# Biblica® Buɗaɗɗen Littafi Mai Tsarki, Sabon Rai Don Kowa™

Hausa: Biblica® Buɗaɗɗen Littafi Mai Tsarki, Sabon Rai Don Kowa™ (Bible) of Nigeria

# Biblica® Buɗaɗɗen Littafi Mai Tsarki, Sabon Rai Don Kowa™
## Hausa: Biblica® Buɗaɗɗen Littafi Mai Tsarki, Sabon Rai Don Kowa™ (Bible) of Nigeria

copyright © 2020 Biblica, Inc.

Language: Hausa

Contributor: Biblica, Inc.

**Biblica® Open Yoruba Contemporary Bible™**
**Copyright © 2009, 2017 by Biblica, Inc.**
Used with permission. All rights reserved worldwide.
"Biblica" is a trademark registered in the United States Patent and Trademark Office by Biblica, Inc. Used with permission.
All content on open.bible is made available under a Creative Commons Attribution-ShareAlike 4.0 License (http://creativecommons.org/licenses/by-sa/4.0/).
You are free to:
Share — copy and redistribute the material in any medium or format
Adapt — remix, transform, and build upon the material for any purpose, even commercially
Under the following conditions:
Attribution — You must attribute the work as follows: "Original work available for free at www.biblica.com and open.bible" Attribution statements in derivative works should not in any way suggest that we endorse you or your use of this work.
ShareAlike — If you remix, transform, or build upon the material, you must distribute your contributions under the same license as the original.
Use of trademarks: Biblica® is a trademark registered in the United States Patent and Trademark Office by Biblica, Inc. and may not be included on any derivative works. Unaltered content from open.bible must include the Biblica® trademark when distributed to others. If you alter the content in any way, you must remove the Biblica® trademark before distributing your work.
This translation is made available to you under the terms of the Creative Commons Attribution Share-Alike license 4.0.
You have permission to share and redistribute this Bible translation in any format and to make reasonable revisions and adaptations of this translation, provided that:
You include the above copyright and source information.
If you make any changes to the text, you must indicate that you did so in a way that makes it clear that the original licensor is not necessarily endorsing your changes.
If you redistribute this text, you must distribute your contributions under the same license as the original.
Pictures included with Scriptures and other documents on this site are licensed just for use with those Scriptures and documents. For other uses, please contact the respective copyright owners.
Note that in addition to the rules above, revising and adapting God's Word involves a great responsibility to be true to God's Word. See Revelation 22:18-19.

2021-11-15

---

PDF generated using Haiola and XeLaTeX on 16 Sep 2023 from source files dated 16 Nov 2021
18113be6-b3a0-530a-b78f-a25225282250

Contents

Farawa . . . 1
Fitowa . . . 66
Firistoci . . . 115
Kidaya . . . 149
Maimaitawar Shari’a . . . 202
Yoshuwa . . . 245
Mahukunta . . . 273
Rut . . . 301
1 Sama’ila . . . 306
2 Sama’ila . . . 343
1 Sarakuna . . . 379
2 Sarakuna . . . 416
1 Tarihi . . . 452
2 Tarihi . . . 497
Ezra . . . 538
Nehemiya . . . 551
Esta . . . 570
Ayuba . . . 579
Zabura . . . 628
Karin Magana . . . 767
Mai Hadishi . . . 818
Waƙar Waƙoƙi . . . 832
Ishaya . . . 842
Irmiya . . . 946
Makoki . . . 1036
Ezekiyel . . . 1049
Daniyel . . . 1112
Hosiya . . . 1131
Yowel . . . 1148
Amos . . . 1155
Obadiya . . . 1168
Yunana . . . 1170
Mika . . . 1173
Nahum . . . 1183
Habakkuk . . . 1188
Zefaniya . . . 1193
Haggai . . . 1199
Zakariya . . . 1201
Malaki . . . 1213
Mattiyu . . . 1217
Markus . . . 1262
Luka . . . 1290
Yohanna . . . 1336
Ayyukan Manzanni . . . 1369
Romawa . . . 1410
1 Korintiyawa . . . 1429
2 Korintiyawa . . . 1446

Galatiyawa . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . 1457
Afisawa . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . 1463
Filibbiyawa . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . 1469
Kolossiyawa . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . 1474
1 Tessalonikawa . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . 1478
2 Tessalonikawa . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . 1482
1 Timoti . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . 1485
2 Timoti . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . 1490
Titus . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . 1494
Filemon . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . 1497
Ibraniyawa . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . 1498
Yaƙub . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . 1512
1 Bitrus . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . 1517
2 Bitrus . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . 1522
1 Yohanna . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . 1525
2 Yohanna . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . 1530
3 Yohanna . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . 1531
Yahuda . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . 1532
Ru’uya ta Yohanna . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . . 1534

# Farawa

*Masomi*

1 A farko-farko, Allah ya halicci sama da ƙasa. 2 To, ƙasa dai ba ta da siffa, babu
kuma kome a cikinta, duhu ne kawai ya rufe ko'ina, Ruhun Allah kuwa yana yawo a
kan ruwan.

3 Sai Allah ya ce, "Bari haske yă kasance," sai kuwa ga haske. 4 Allah ya ga hasken
yana da kyau, sai ya raba tsakanin hasken da duhu. 5 Allah ya kira hasken "yini," ya
kuma kira duhun "dare." Yamma ta kasance, safiya kuma ta kasance, kwana ta fari
ke nan.

6 Allah ya ce, "Bari sarari yă kasance tsakanin ruwaye domin yă raba ruwa da
ruwa." 7 Saboda haka Allah ya yi sarari ya raba ruwan da yake ƙarƙashin sararin
da ruwan da yake bisansa. Haka kuwa ya kasance. 8 Allah ya kira sararin "sama."
Yamma ta kasance, safiya kuma ta kasance, kwana ta biyu ke nan.

9 Allah ya ce, "Bari ruwan da yake ƙarƙashin sama yă tattaru wuri ɗaya, bari kuma
busasshiyar ƙasa tă bayyana." Haka kuwa ya kasance. 10 Allah ya kira busasshiyar
ƙasar "doron ƙasa," ruwan da ya taru kuma, ya kira "tekuna." Allah ya ga yana da
kyau.
11 Sa'an nan Allah ya ce, "Bari ƙasa tă fid da tsire-tsire, da shuke-shuke, da itatuwa
a bisa ƙasa masu ba da amfani da 'ya'ya a cikinsu, bisa ga irinsu." Haka kuwa ya
kasance. 12 Kasar ta fid da tsire-tsire, da shuke-shuke masu ba da 'ya'ya bisa ga irinsu,
ta fid kuma da itatuwa masu ba da 'ya'ya da iri a cikinsu bisa ga irinsu. Allah ya ga
yana da kyau. 13 Yamma ta kasance, safiya kuma ta kasance, kwana ta uku ke nan.

14 Allah kuma ya ce, "Bari haskoki su kasance a sararin sama domin su raba yini da
dare, bari su zama alamu domin su nuna yanayi, da ranaku, da kuma shekaru, 15 bari
kuma haskokin su kasance a sararin sama domin su ba da haske a duniya." Haka
kuwa ya kasance. 16 Allah ya yi manyan haskoki biyu, babban hasken yă mallaki
yini, ƙaramin kuma yă mallaki dare. Ya kuma yi taurari. 17 Allah ya sa su a sararin
sama domin su ba da haske a duniya, 18 su mallaki yini da kuma dare, su kuma raba
haske da duhu. Allah kuwa ya ga yana da kyau. 19 Yamma ta kasance, safiya kuma
ta kasance, kwana ta huɗu ke nan.

20 Allah ya ce, "Bari ruwa yă cika da halittu masu rai, bari tsuntsaye kuma su tashi
sama a bisa duniya a sararin sama." 21 Allah ya halicci manyan halittun teku, da
kowane mai rai da abin da yake motsi a ruwa, bisa ga irinsu, da kuma kowane tsuntsu
mai fiffike bisa ga irinsa. Allah kuwa ya ga yana da kyau. 22 Allah ya albarkace su
ya ce, "Ku yi ta haihuwa ku kuma ƙaru da yawa, ku cika ruwan tekuna, bari kuma
tsuntsaye su yi yawa a bisa duniya." 23 Yamma ta kasance, safiya kuma ta kasance,
kwana ta biyar ke nan.

24 Allah kuwa ya ce, "Bari ƙasa tă ba da halittu masu rai bisa ga irinsu; dabbobi
da halittu masu rarrafe, da kuma namun jeji, kowane bisa ga irinsa." Haka kuwa ya
kasance. 25 Allah ya halicci namun jeji bisa ga irinsu, dabbobi bisa ga irinsu, da kuma
dukan halittu masu rarrafe a ƙasa bisa ga irinsu. Allah kuwa ya ga yana da kyau.

26 Sa'an nan Allah ya ce, "Bari mu yi mutum cikin siffarmu, cikin kamanninmu,
bari kuma su yi mulki a bisa kifin teku, tsuntsayen sama, da kuma dabbobi, su yi
mulki a bisa dukan duniya, da kuma a bisa dukan halittu, da masu rarrafe a ƙasa."
27 Saboda haka Allah ya halicci mutum cikin siffarsa.
Cikin kamannin Allah, Allah ya halicci mutum.
Miji da mace ya halicce su.
28 Allah ya albarkace su, ya kuma ce musu, "Ku yi ta haihuwa ku ƙaru da yawa, ku
mamaye duniya, ku mallake ta. Ku yi mulki a bisa kifin teku, da tsuntsayen sararin
sama, da kuma bisa kowace halitta mai rai wadda take rarrafe a ƙasa."
29 Sa'an nan Allah ya ce, "Ga shi, na ba ku kowane tsiro mai ba da 'ya'ya masu
kwaya da suke a fāɗin duniya, da dukan itatuwa masu ba da 'ya'ya, don su zama
abinci a gare ku. 30 Na kuma ba da dukan dabbobin ƙasa, da dukan tsuntsayen sama,
da dukan abin da yake rarrafe a ƙasa, da dai iyakar abin da yake numfashi; haka
kuma na ba da ganyaye su zama abinci." Haka kuwa ya kasance.
31 Allah ya ga dukan abin da ya yi, yana da kyau ƙwarai. Yamma ta kasance, safiya
kuma ta kasance, kwana ta shida ke nan.

# 2

1 Ta haka aka gama yin sammai da duniya da dukan abubuwan da suke cikinsu.

2 Kafin kwana ta bakwai, Allah ya gama aikin da yake yi, saboda haka a kwana ta
bakwai, ya huta daga dukan aikinsa. 3 Allah kuwa ya albarkaci kwana ta bakwai, ya
kuma mai da ita mai tsarki, saboda a kanta ne ya huta daga dukan aikin halittar da
ya yi.

### *Adamu da Hawwa'u*

4 Wannan shi ne asalin tarihin sammai da duniya sa'ad da aka halicce su.

Sa'ad da Ubangiji Allah ya yi duniya da sammai, 5 babu tsiro a duniya kuma
ganyaye ba su tsira a busasshiyar ƙasa ko ba, gama Ubangiji Allah bai aiko da ruwan
sama a kan duniya ba tukuna, babu kuma wani mutumin da zai nome ƙasar, 6 amma
dai rafuffuka suna ɓullo da ruwa daga ƙasa suna jiƙe ko'ina a fāɗin ƙasa. 7 Sa'an
nan Ubangiji Allah ya yi mutum daga turɓayar ƙasa, ya kuma hura numfashin rai
cikin hancinsa, mutumin kuwa ya zama rayayyen taliki.
8 To, fa, Ubangiji Allah ya yi lambu a gabas, a Eden, a can kuwa ya sa mutumin da
ya yi. 9 Ubangiji Allah ya kuma sa kowane irin itace ya tsira daga ƙasa, itace mai
kyan gani, mai amfani kuma don abinci. A tsakiyar lambun kuwa akwai itacen rai
da kuma itacen sanin abin da yake da kyau da abin da yake mugu.
10 Akwai wani kogi mai ba da ruwa ga lambun wanda ya gangaro daga Eden, daga
nan ya rarrabu, ya zama koguna huɗu. 11 Sunan kogi na fari, Fishon. Shi ne yake
malala kewaye da dukan ƙasar Hawila, inda akwai zinariya. 12 (Zinariyar wannan
ƙasa kuwa tana da kyau, akwai kuma kayan ƙanshi da duwatsun da ake kira onis
a can ma.) 13 Sunan kogi na biyu, Gihon. Shi ne ya malala kewaye da ƙasar Kush.*
14 Sunan kogi na uku Tigris. Wannan ne ya malala ya bi ta gefen gabashin Asshur.
Kogi na huɗu kuwa shi ne Yuferites.
15 Ubangiji Allah ya ɗauko mutumin ya sa shi cikin Lambun Eden domin yǎ nome
shi, yǎ kuma lura da shi. 16 Ubangiji Allah ya umarci mutumin ya ce, "Kana da 'yanci
ka ci daga kowane itace a cikin lambun, 17 amma kada ka ci daga itacen sanin abin
da yake mai kyau da abin da yake mugu, gama a ranar da ka ci shi, lalle za ka mutu."

* **2:13** Mai yiwuwa kudu maso gabas na Mesofotamiya ne

[18] UBANGIJI Allah ya ce, “Bai yi kyau mutumin yă kasance shi kaɗai ba. Zan yi masa mataimakin da ya dace da shi.”
[19] To, UBANGIJI Allah ya yi dukan namun jeji da dukan tsuntsayen sama daga ƙasa. Ya kawo su wurin mutumin don yă ga wanda suna zai kira su; kuma duk sunan da mutumin ya kira kowane mai rai, sunansa ke nan. [20] Saboda haka mutumin ya sa wa dukan dabbobi, da tsuntsayen sama da dukan namun jeji sunaye.
Amma ba a sami mataimakin da ya dace da Adamu ba. [21] Saboda haka UBANGIJI Allah ya sa mutumin ya yi barci mai nauyi; yayinda yake barci sai ya ɗauko ɗaya daga cikin haƙarƙarin mutumin, ya kuma rufe wurin da nama. [22] Sa'an nan UBANGIJI Allah ya yi mace daga haƙarƙarin da ya ɗauko daga mutumin, ya kuwa kawo ta wurin mutumin.
[23] Sai mutumin ya ce,
“Yanzu kam wannan ƙashi ne na ƙasusuwana
nama kuma na namana.
Za a ce da ita ‘mace,’
gama an ciro ta daga namiji.”
[24] Wannan ne ya sa mutum yakan bar mahaifinsa da mahaifiyarsa, yă manne wa matarsa, su kuma zama jiki ɗaya.
[25] Mutumin da matarsa, dukansu biyu tsirara suke, ba su kuwa ji kunya ba.

# 3

*Fāɗuwar mutum*

[1] To, maciji dai ya fi kowane a cikin namun jejin da UBANGIJI Allah ya yi wayo. Ya ce wa macen, “Tabbatacce ne Allah ya ce, ‘Kada ku ci daga kowane itace a lambu’?”
[2] Macen ta ce wa macijin, “Za mu iya ci daga 'ya'ya itatuwa a lambun, [3] amma Allah ya ce, ‘Kada ku ci daga 'ya'yan itacen da yake tsakiyar lambu, kada kuma ku taɓa shi, in ba haka ba kuwa za ku mutu.’ ”
[4] Maciji ya ce wa macen, “Tabbatacce ba za ku mutu ba. [5] Gama Allah ya san cewa sa'ad da kuka ci daga itacen idanunku za su buɗe, za ku kuma zama kamar Allah, ku san abin da yake mai kyau da abin da yake mugu.”
[6] Sa'ad da macen ta ga 'ya'yan itacen suna da kyau don abinci, abin sha'awa ga ido, abin marmari kuma don samun hikima, sai ta tsinka ta ci, ta kuma ba da waɗansu wa mijinta wanda yake tare da ita, shi ma ya ci. [7] Sa'an nan idanun dukansu biyu suka buɗe, suka kuma gane tsirara suke; saboda haka suka ɗinɗinka ganyayen ɓaure suka yi wa kansu sutura.
[8] Da mutumin da matarsa suka ji motsin UBANGIJI Allah yana takawa a lambun a sanyin yini, sai suka ɓuya daga UBANGIJI Allah a cikin itatuwan lambu. [9] Amma UBANGIJI Allah ya kira mutumin ya ce, “Ina kake?”
[10] Ya ce, “Na ji ka a cikin lambu, na kuwa ji tsoro gama ina tsirara, saboda haka na ɓuya.”
[11] Sai ya ce, “Wa ya faɗa maka cewa kana tsirara? Ko dai ka ci daga itacen da na umarce ka kada ka ci ne?”
[12] Mutumin ya ce, “Macen da ka sa a nan tare da ni, ita ta ba ni waɗansu 'ya'ya daga itacen, na kuwa ci.”
[13] Sai UBANGIJI Allah ya ce wa matar, “Me ke nan kika yi?”
Matar ta ce, “Macijin ne ya ruɗe ni, na kuwa ci.”
[14] Saboda haka UBANGIJI Allah ya ce wa macijin, “Saboda ka yi haka,
“Na la'anta ka cikin dukan dabbobi da kuma cikin dukan namun jeji!
Daga yanzu rubda ciki za ka yi tafiya
turɓaya kuma za ka ci
dukan kwanakin rayuwarka.

15 Zan kuma sa ƙiyayya
tsakaninka da macen,
tsakanin zuriyarka da zuriyarta.
Zai ragargaje kanka,
kai kuma za ka sari ɗiɗɗigensa.”
16 Sa’an nan ya ce wa macen,
“Zan tsananta naƙudarki ainun,
da azaba kuma za ki haifi ’ya’ya.
Za ki riƙa yin marmarin mijinki
zai kuwa yi mulki a kanki.”
17 Ga Adamu kuwa ya ce, “Saboda ka saurari matarka, ka kuma ci daga itacen da
na ce, ‘Kada ka ci,’
“Za a la’anta ƙasa saboda kai.
Da wahala za ka ci daga cikinta dukan kwanakin rayuwarka.
18 Za tă ba ka ƙayayyuwa da sarƙaƙƙiya
za ka kuwa ci ganyayen gona.
19 Da zuffan goshinka za ka ci abincinka har ka koma ga ƙasa,
da yake daga cikinta aka yi ka.
Gama kai turɓaya ne,
kuma ga turɓaya za ka koma.”
20 Mutumin ya sa wa matarsa suna, Hawwa’u, gama za tă zama mahaifiyar masu
rai duka.
21 UBANGIJI Allah ya yi tufafin fata domin Adamu da Hawwa’u, ya kuma yi musu
sutura. 22 UBANGIJI Allah ya kuma ce, “To, fa, mutum ya zama kamar ɗaya daga
cikinmu, ya san abin da yake mai kyau da abin da yake mugu. Kada a yarda yă miƙa
hannunsa yă ɗiba daga itacen rai yă ci, yă kuma rayu har abada.” 23 Saboda haka
UBANGIJI Allah ya kore shi daga Lambun Eden domin yă nome ƙasa wadda aka yi shi.
24 Bayan da ya kori mutumin, sai ya sa kerubobi da takobi mai harshen wuta yana
jujjuyawa baya da gaba a gabashin Lambun Eden don yă tsare hanya zuwa itacen
rai.

# 4

### *Kayinu da Habila*

1 Adamu ya kwana da matarsa Hawwa’u, ta kuwa yi ciki ta haifi Kayinu. Sai ta
ce, “Da taimakon UBANGIJI na sami ɗa namiji.” 2 Daga baya ta haifi ɗan’uwansa, ta
kuma ba shi suna Habila.
Sa’ad da suka yi girma sai Habila ya zama makiyayin tumaki, Kayinu kuwa ya zama
manomi. 3 Ana nan sai Kayinu ya kawo waɗansu amfanin gona a matsayin hadaya ga
UBANGIJI. 4 Amma Habila ya kawo mafi kyau daga ’ya’yan fari na garkensa. UBANGIJI
ya yi farin ciki da sadakar da Habila ya kawo, 5 amma bai yi farin ciki da sadakar da
Kayinu ya kawo ba. Saboda haka Kayinu ya ji fushi sosai, fuskarsa kuma ta ɓace.
6 Sai UBANGIJI ya ce wa Kayinu, “Don me kake fushi? Don me fuskarka ta ɓace?
7 Da ka yi abin da yake daidai, ai, da ka sami karɓuwa. Amma tun da ba ka yi abin
da ba daidai ba, zunubi zai yi fakonka don yă rinjaye ka kamar naman jeji. Yana so
yă mallake ka, amma tilas ka rinjaye shi.”
8 To, Kayinu ya ce wa ɗan’uwansa Habila, “Mu tafi gona.”* Yayinda suke a gona,
sai Kayinu ya tasar wa Habila ya buge shi ya kashe.
9 Sai UBANGIJI ya ce wa Kayinu, “Ina ɗan’uwanka Habila?”

* **4:8** Rubuce-rubucen hannu na Fentatut na Samariyawa, Seftuwajin, Bulget da Siriyak; Rubuce-rubucen hannu na Masoretik ba su da “Mu tafi gona.”

Sai Kayinu ya ce, “Ban sani ba, ni mai gadin ɗan’uwana ne?”
10 UBANGIJI ya ce, “Me ke nan ka yi? Saurara! Ga jinin ɗan’uwanka yana mini kuka
daga ƙasa. 11 Yanzu, kai la’ananne ne, an kuma kore ka daga ƙasa wadda ta buɗe
bakinta ta shanye jinin ɗan’uwanka daga hannunka. 12 In ka nome ƙasa, ba za tă
ƙara ba ka hatsinta ba. Za ka kuma zama mai yawo barkatai a duniya.”
13 Kayinu ya ce wa UBANGIJI, “Horon nan ya sha ƙarfina. 14 Ga shi, yau kana kori
na daga ƙasar, zan zama a ɓoye daga fuskarka, zan kuma zama mai yawo barkatai,
duk wanda ya same ni kuwa zai kashe ni.”
15 Amma UBANGIJI ya ce masa, “Ba haka ba ne! Duk wanda ya kashe Kayinu, za a
ninƙa hukuncinsa har sau bakwai.” Sa’an nan UBANGIJI ya sa wa Kayinu alama don
duk wanda ya same shi kada yă kashe shi. 16 Saboda haka Kayinu ya yi tafiyarsa ya
rabu da UBANGIJI, ya je ya zauna ƙasar Nod† a gabashin Eden.
17 Kayinu ya kwana da matarsa, ta kuwa yi ciki, ta haifi Enok. A lokacin Kayinu
yana gina birni, sai ya sa wa birnin sunan ɗansa Enok. 18 Aka haifa wa Enok Irad, Irad
kuma ya haifi Mehujayel, Mehujayel kuma ya haifi Metushayel, Metushayel kuma ya
haifin Lamek.
19 Lamek ya auri mata biyu, ana ce da ɗaya Ada, ɗayan kuma Zilla. 20 Ada ta haifi
Yabal, shi ne mahaifi waɗanda suke zama a tentuna, suna kuma kiwon dabbobi.
21 Sunan ɗan’uwansa Yubal, shi ne mahaifin dukan makaɗan garaya da masu hura
sarewa. 22 Zilla ma ta haifi ɗa, Tubal-Kayinu, shi ne wanda ya ƙera kowane iri kayan
aiki daga tagulla da kuma ƙarfe. ’Yar’uwar Tubal-Kayinu ita ce Na’ama.
23 Wata rana, Lamek ya ce wa matansa, Ada da Zilla,

“Ku saurara, matan Lamek, ku ji maganata.
Na kashe‡ wani saboda ya yi mini rauni,
na kashe wani saurayi saboda ya ji mini ciwo.
24 Idan za a rama wa Kayinu har sau bakwai,
lalle za a rama wa Lamek sau saba’in da bakwai ke nan.”

25 Sai Adamu ya sāke kwana da matarsa, ta haifi ɗa, aka kuma ba shi suna Set,
gama ta ce, “Allah ya ba ni wani yaro a madadin Habila, tun da yake Kayinu ya
kashe shi.” 26 Set ma ya haifi ɗa, ya kuma kira shi Enosh.
A lokaci ne, mutane suka fara kira ga sunan UBANGIJI.

# 5

*Daga Adamu zuwa Nuhu*

1 Wannan shi ne rubutaccen tarihin zuriyar Adamu.

Sa’ad da Allah ya halicci mutum, ya yi shi cikin kamannin Allah. 2 Ya halicce su
namiji da ta mace, ya kuma albarkace su. Sa’ad da kuma aka halicce su, ya kira su
“Mutum.”*

3 Sa’ad da Adamu ya yi shekaru 130, sai ya haifi ɗa wanda ya yi kama da shi, ya
kuma kira shi Set. 4 Bayan an haifi Set, Adamu ya yi shekaru 800, ya kuma haifi
waɗansu ’ya’ya maza da mata. 5 Gaba ɗaya dai, Adamu ya yi shekaru 930, sa’an
nan ya mutu.
6 Sa’ad da Set ya yi shekara 105, sai ya haifi Enosh. 7 Bayan ya haifi Enosh, Set ya
yi shekara 807, ya kuma haifi waɗansu ’ya’ya maza da mata. 8 Gaba ɗaya dai,
Set ya yi shekaru 912, sa’an nan ya mutu.

† **4:16** Nod yana nufin yawo (dubi ayoyi 12 da 14). ‡ **4:23** Ko kuwa zan kashe * **5:2** Da Ibraniyanci adam

[9] Sa'ad da Enosh ya yi shekara 90, sai ya haifi Kenan. [10] Bayan ya haifi Kenan,
Enosh ya yi shekara 815, ya kuma haifi waɗansu 'ya'ya maza da mata. [11] Gaba
ɗaya dai, Enosh ya yi shekaru 905, sa'an nan ya mutu.
[12] Sa'ad da Kenan ya yi shekara 70, sai ya haifi Mahalalel. [13] Bayan ya haifi
Mahalalel, Kenan ya yi shekara 840, ya kuma haifi waɗansu 'ya'ya maza da mata
[14] Gaba ɗaya dai, Kenan ya yi shekara 910, sa'an nan ya mutu.
[15] Sa'ad da Mahalalel ya yi shekara 65, sai ya haifi Yared. [16] Bayan ya haifi Yared,
Mahalalel ya yi shekara 830, ya kuma haifi waɗansu 'ya'ya maza da mata [17] Gaba
ɗaya dai, Mahalalel ya yi shekara 895, sa'an nan ya mutu.
[18] Sa'ad da Yared ya yi shekara 162, sai ya haifi Enok. [19] Bayan ya haifi Enok, Yared
ya yi shekaru 800, ya kuma haifi waɗansu 'ya'ya maza da mata. [20] Gaba ɗaya
dai, Yared ya yi shekara 962, sa'an nan ya mutu.
[21] Sa'ad da Enok ya yi shekara 65, sai ya haifi Metusela. [22] Bayan ya haifi Metusela,
Enok ya kasance cikin zumunci da Allah shekaru 300, ya kuma haifi waɗansu
'ya'ya maza da mata. [23] Gaba ɗaya dai, Enok ya yi shekaru 365. [24] Enok ya
kasance cikin zumunci da Allah, sa'an nan ba a ƙara ganinsa ba. Saboda Allah
ya ɗauke shi.
[25] Sa'ad da Metusela ya yi shekara 187, sai ya haifi Lamek. [26] Bayan ya haifi Lamek,
Metusela ya yi shekaru 782, ya kuma haifi waɗansu 'ya'ya maza da mata. [27] Gaba
ɗaya dai, Metusela ya yi shekaru 969, sa'an nan ya mutu.
[28] Sa'ad da Lamek ya yi shekara 182, sai ya haifi ɗa. [29] Ya ba shi suna Nuhu† ya
kuma ce, "Zai yi mana ta'aziyya a cikin aikinmu da wahalar hannuwanmu a
ƙasar da UBANGIJI ya la'anta." [30] Bayan an haifi Nuhu, Lamek ya yi shekara 595,
yana kuma da 'ya'ya maza da mata. [31] Gaba ɗaya dai, Lamek ya yi shekaru 777,
sa'an nan ya mutu.
[32] Bayan Nuhu ya yi shekara 500, sai ya haifi Shem, Ham da Yafet.

# 6

*Mugunta a duniya*

[1] Sa'ad da mutane suka fara ƙaruwa a duniya, aka kuma hahhaifi musu 'ya'ya mata,
[2] sai 'ya'yan Allah maza suka ga cewa 'ya'yan mutane mata suna da bansha'awa, sai
suka zaɓi waɗanda suke so, suka aura. [3] Sa'an nan UBANGIJI ya ce, "Ruhuna ba zai
zauna a cikin mutum har abada ba, saboda shi mai mutuwa ne, kwanakinsa za su
zama shekaru ɗari da arba'in ne."
[4] Nefilimawa suna nan a duniya a waɗancan kwanaki, da kuma kwanakin da suka
bi baya, a sa'ad da 'ya'yan Allah suka kwana da 'ya'yan mutane mata, suka kuma
hahhaifi musu 'ya'ya. Ai, su ne jarumawan dā, mutanen da suka shahara.
[5] UBANGIJI kuwa ya lura cewa muguntar mutum ta yi yawa a duniya, kuma kowane
abin da yake tunani a zuciyarsa mugu ne kawai a kowanne lokaci. [6] UBANGIJI ya
damu da ya yi mutum a duniya, abin ya zafe shi ƙwarai. [7] Saboda haka UBANGIJI
ya ce, "Zan kawar da mutum, da dabbobi, da halittu masu rarrafe a ƙasa da kuma
tsuntsayen sama waɗanda na halitta, daga doron ƙasa, saboda na damu da na yi su."
[8] Amma Nuhu ya sami tagomashi a gaban UBANGIJI.

[9] Ga tarihin Nuhu.

Nuhu mutum ne mai adalci, marar abin zargi a cikin mutanen zamaninsa, ya kuma
yi tafiya tare da Allah. [10] Nuhu yana da 'ya'ya maza uku, Shem, Ham da Yafet.

† **5:29** Nuhu ya yi kama da kalmar Ibraniyancin nan na ta'aziyya.

[11] Duniya dai ta lalace sosai a gaban Allah, ta kuma cika da tashin hankali. [12] Allah
ya ga yadda duniya ta lalace, gama dukan mutane a duniya sun lalatar da rayuwarsu.
[13] Saboda haka, Allah ya ce wa Nuhu, “Zan kawo ƙarshen dukan mutane, gama
saboda su duniya ta cika da tashin hankali. Lalle zan hallaka su da kuma duniya.
[14] Saboda haka ka yi wa kanka jirgi da katakon Saifires*, ka yi ɗakuna a cikinsa, ka
shafe shi da ƙaro ciki da waje. [15] Ga yadda za ka gina shi; jirgin zai kasance mai
tsawon ƙafa 45, fāɗinsa ƙafa 75, tsayinsa kuma ƙafa 45. [16] Ka yi masa rufi, ka kuma
ba da fili inci 18 tsakanin rufin a kowane gefen jirgin.† Ka sa ƙofa a gefen jirgin. Ka
yi shi hawa uku, ka yi ƙofa a gefe. [17] Ga shi zan aiko da ambaliya ruwa a duniya, in
hallaka dukan mai rai da yake a ƙarƙashin sama, kowace halittar da take numfashi
a cikinta. Dukan abin da yake a duniya zai hallaka. [18] Amma zan kafa alkawarina
da kai, kai kuma za ka shiga jirgin, kai da ’ya’yanka maza da matarka da matan
’ya’yanka tare da kai. [19] Za ka shigar da biyu na dukan halittu masu rai, namiji da
ta mace a cikin jirgin, domin su rayu tare da kai. [20] Biyu na kowane irin tsuntsu,
kowace irin dabba da kuma kowace irin halitta mai rarrafe a ƙasa, za su zo wurinka
domin a bar su da rai. [21] Za ka ɗauki kowane irin abinci wanda za a ci, ka adana
don yă zama abincinka da nasu.”
[22] Nuhu ya yi kome kamar yadda Allah ya umarce shi.

# 7

[1] Sa’an nan Ubangiji ya ce wa Nuhu. “Shiga jirgin, kai da dukan iyalinka, gama na
ga kai mai adalci ne a wannan zamani. [2] Ka ɗauki bakwai na kowace iri tsabtaccen
dabba tare da kai, namiji da ta mace, da kuma biyu na kowace dabba marar tsabta,
namiji da ta mace, [3] da kuma bakwai na kowane iri tsuntsu, namiji da ta mace, domin
a bar kowane irinsu da rai a dukan duniya. [4] Kwana bakwai daga yanzu zan aiko da
ruwa a duniya yini arba’in da dare arba’in, zan kuma kawar da kowace halitta mai
rai da na yi daga doron ƙasa.”
[5] Nuhu ya aikata duk abin da Ubangiji ya umarce shi.
[6] Nuhu yana da shekaru 106 ne sa’ad da aka yi ambaliya ruwa a duniya. [7] Nuhu da
matarsa da ’ya’yansa da matansu, suka shiga jirgi domin su tsira daga ruwa ambaliya.
[8] Biyu-biyu daga dabbobi masu tsabta da marasa tsabta, da tsuntsaye da kuma dukan
halittu masu rarrafe a ƙasa, [9] namiji da ta mace, suka zo wurin Nuhu, suka shiga
jirgi, kamar yadda Allah ya umarce Nuhu. [10] Bayan kwana bakwai kuwa ambaliya
ruwa ta sauko a bisa duniya.
[11] A ranar sha bakwai ga wata na biyu, na shekara ta ɗari shida na rayuwar Nuhu,
a ran nan sai dukan maɓuɓɓugai na manyan zurfafa suka fashe, tagogin sammai
suka buɗe. [12] Ruwa yana ta kwararowa bisa duniya, yini arba’in da dare arba’in.
[13] A wannan rana Nuhu tare da matarsa da ’ya’yansa maza, Shem, Ham da Yafet da
matansu uku suka shiga jirgi. [14] Tare da su kuwa, akwai kowane naman jeji bisa ga
irinsa, da dukan dabbobin gida bisa ga irinsu, da kowace halitta mai rarrafe a ƙasa
bisa ga irinta, da kowane tsuntsun gida da na jeji bisa ga irinsa, da dukan abu mai
fiffike. [15] Biyu-biyu na dukan halittu masu numfashi suka zo wurin Nuhu, suka shiga
jirgi. [16] Dabbobi da kowane abu mai rai da suka shiga ciki, namiji ne da ta mace,
yadda Allah ya umarci Nuhu. Sa’an nan Ubangiji ya kulle jirgin daga baya.
[17] Kwana arba’in ambaliya ta yi ta saukowa a duniya, sa’ad da ruwa ya yi ta ƙaruwa
sai ya yi ta ɗaga jirgin sama, ya kuwa tashi can bisa duniya. [18] Ruwa ya taso, ya ƙaru
ƙwarai a duniya, jirgin kuma ya yi ta yawo a bisa ruwa. [19] Ruwa ya ƙaru ƙwarai a
duniya, ya kuma rufe dukan duwatsu masu tsawo a ƙarƙashin sammai. [20] Ruwan

* **6:14** Babu tabbas game da ma’anar kalman nan a Ibraniyanci. † **6:16** Ko kuwa Ka bar inda haske zai shiga ta wurin gamawa

ya taso ya rufe duwatsu, zurfin ruwa daga duwatsun zuwa inda jirgin yake ya fi
ƙafa ashirin. 21 Kowane abu mai rai da yake tafiya a duniya ya hallaka, tsuntsaye,
dabbobin gida, namun jeji, da dukan masu rarrafe waɗanda suke rarrafe a duniya,
da kuma dukan mutane. 22 Kome a busasshiyar ƙasa da yake numfashi a hancinsa
ya mutu. 23 Aka kawar da kowane abu mai rai, mutane da dabbobi da halittu masu
rarrafe a ƙasa, da tsuntsayen sama a doron ƙasa, duka aka kawar da su daga duniya.
Nuhu kaɗai aka bari da waɗanda suke tare da shi a cikin jirgi.

24 Ruwa ya mamaye duniya har kwana ɗari da hamsin.

# 8

1 Amma Allah ya tuna da Nuhu da dukan namun jeji da dabbobin da suke tare
da shi a cikin jirgi, ya kuma aika da wata iska ta hura dukan duniya, ruwan kuwa
ya janye. 2 Aka toshe maɓuɓɓugan zurfafa da ƙofofin ambaliyar sammai, ruwan
sama kuma ya daina saukowa daga sarari. 3 Ruwan ya janye a hankali daga ƙasa. A
ƙarshen kwanaki ɗari da hamsin ɗin, ruwan ya ragu. 4 A rana ta goma sha bakwai
ga watan bakwai, jirgin ya sauka a duwatsun Ararat. 5 Ruwan ya ci gaba da janyewa
har watan goma. A rana ta fari ga watan goma kuwa ƙwanƙolin duwatsun suka
bayyana.

6 Bayan kwana arba'in, sai Nuhu ya buɗe tagar jirgin da ya yi, 7 ya saki hankaka.
Hankaka ya yi ta kai da kawowa har sai da ruwa ya shanye a duniya. 8 Sai ya saki
kurciya don yă ga in ruwan ya janye daga doron ƙasa. 9 Amma kurciyar ba tă sami
inda za tă sa ƙafafunta ba gama akwai ruwa a dukan doron ƙasa, saboda haka ta
komo wurin Nuhu a jirgi. Ya miƙa hannunsa ya ɗauko kurciyar ya shigar da ita
wurinsa a cikin jirgi. 10 Ya ƙara jira kwana bakwai, sai ya sāke aiken kurciyar daga
jirgi. 11 Sa'ad da kurciya ta komo wurinsa da yamma, sai ga ɗanyen ganyen zaitun
da ta tsinko a bakinta! Sa'an nan Nuhu ya san cewa ruwa ya janye daga duniya.
12 Ya ƙara jira kwana bakwai, sai ya sāke aiken kurciyar, amma a wannan ƙaro ba
tă komo wurinsa ba.

13 A rana ta fari ga wata na fari wanda Nuhu ya cika shekaru 601, ruwa ya shanye
a ƙasa. Sai Nuhu ya buɗe murfin jirgin, ya ga cewa doron ƙasa ya bushe. 14 A ran
ashirin da bakwai ga wata na biyu, ƙasa ta bushe ƙaƙaf.

15 Sa'an nan Allah ya ce wa Nuhu, 16 "Fito daga jirgin, kai da matarka da 'ya'yanka
maza da matansu. 17 Ka fitar da kowane iri halitta mai rai da take tare da kai waje,
tsuntsaye, dabbobi, da dukan halittu masu rarrafe a ƙasa, don su yi ta haihuwa, su
yi yawa, su ƙaru a duniya."

18 Sai Nuhu ya fito tare da matarsa da 'ya'yansa maza da matan 'ya'yansa, 19 da
kowace irin dabba, da kowane mai rarrafe, da kowane irin tsuntsu, da kowane irin
abu da yake tafiya a bisa duniya, suka fito daga jirgi daki-daki bisa ga irinsu.

20 Sai Nuhu ya gina bagaden hadaya ga UBANGIJI, ya ɗiba waɗansu dabbobi da
tsuntsaye masu tsabta, ya yi hadaya ta ƙonawa da su a kan bagaden. 21 Da UBANGIJI
ya ji ƙanshi mai daɗi, sai ya ce a zuciyarsa, "Ba zan ƙara la'anta ƙasa saboda mutum
ba, ko da yake dukan tunanin zuciyar mutum mugu ne tun yana ƙarami. Ba kuwa
zan ƙara hallaka dukan halittu masu rai, kamar yadda na yi ba.

22 "Muddin duniya tana nan,
lokacin shuki da na girbi,
lokacin sanyi da na zafi,
lokacin damina da na rani,
dare da rana
ba za su daina ba."

# 9

*Alkawarin Allah da Nuhu*

1 Sa'an nan Allah ya sa wa Nuhu da 'ya'yansa maza albarka, yana ce musu, "Ku
haifi 'ya'ya, ku ƙaru, ku kuma cika duniya. 2 Dukan namun jeji da dukan tsuntsayen
sama da kowace halitta mai rarrafe a ƙasa, da dukan kifayen teku, za su riƙa jin
tsoronku, suna fargaba. An sa su a cikin hannuwanku. 3 Kome da yake da rai wanda
yake tafiya, zai zama abincinku. Kamar yadda na ba ku kowane irin ganye, haka na
ba ku kome da kome.
4 "Akwai abu ɗaya da ba za ku ci ba, wato, nama wanda jininsa yake cikinsa
tukuna. 5 Game da jinin ranka kuwa lalle zan bukaci lissafi. Zan bukaci lissafi daga
kowane dabba. kuma daga kowane mutum, shi ma zan bukaci lissafi game da ran
ɗan'uwansa.
6 "Duk wanda ya zub da jinin mutum,
ta hannun mutum za a zub da jininsa;
gama a cikin siffar Allah ne,
Allah ya yi mutum.
7 Amma ku, ku yi ta haihuwa, ku ƙaru; ku yaɗu a duniya, ku yi yawa a bisanta."
8 Sai Allah ya ce wa Nuhu da 'ya'yansa, 9 "Yanzu na kafa alkawarina da ku da
zuriyarku a bayanku, 10 da kowace halitta mai rai wadda ta kasance tare da kai;
wato, tsuntsaye da dabbobin gida da kuma dukan namun jeji, duk dai iyakar abin da
ya fita daga jirgin; wato, kowane mai rai na duniya. 11 Na kafa alkawarina da ku, ba
za a ƙara hallaka dukan rayuka da ambaliyar ruwa ba; ba za a ƙara yin ambaliya
don a hallaka duniya ba."
12 Allah ya kuma ce, "Wannan ita ce alamar alkawarin da na yi tsakanina da ku, da
kowace halitta tare da ku; alkawari na dukan zamanai masu zuwa. 13 Na sa bakan
gizona cikin gizagizai, shi ne kuwa zai zama alamar alkawari tsakanina da duniya.
14 Duk sa'ad da na kawo gizagizai a bisa duniya, bakan gizo kuma ya bayyana a ciki
gizagizan, 15 zan tuna da alkawari tsakanina da ku da kuma dukan halittu masu rai
na kowane iri. Ruwa ba zai sāke yin ambaliyar da za tă hallaka dukan masu rai ba.
16 Duk sa'ad da bakan gizo ya bayyana cikin gizagizan, zan gan shi in kuma tuna da
madawwamin alkawari tsakanin Allah da dukan halittu masu rai, na kowane iri a
duniya."
17 Saboda haka Allah ya ce wa Nuhu, "Wannan ita ce alamar alkawarin da na kafa
tsakanina da dukan masu rai a duniya."

*'Ya'yan Nuhu maza*

18 'Ya'yan Nuhu maza, waɗanda suka fito daga cikin jirgi, su ne, Shem, Ham da
Yafet. (Ham shi ne mahaifin Kan'ana.) 19 Waɗannan su ne 'ya'yan Nuhu maza uku,
daga gare su ne kuma duniya za tă cika da mutane.
20 Nuhu, mutumin ƙasa, shi ne farko da ya fara yin gonar inabi. 21 Sa'ad da
ya sha ruwan inabin ya kuwa bugu, sai ya kwanta tsirara cikin tentinsa. 22 Ham,
mahaifin Kan'ana ya ga tsiraici mahaifinsa, ya kuma faɗa wa 'yan'uwansa biyu a
waje. 23 Amma Shem da Yafet suka ɗauki mayafi, suka shimfiɗa a kafaɗarsu, sa'an
nan suka shiga suna tafiya da baya har zuwa inda mahaifinsu yake kwance, suka
rufe tsiraicinsa. Suka kau da fuskokinsu domin kada su ga tsiraicin mahaifinsu.
24 Sa'ad da Nuhu ya farka daga buguwarsa ya kuma gane abin da ƙarami ɗansa
ya yi, 25 sai ya ce,
"Kan'ana la'ananne ne,
zai zama bawa mafi ƙanƙanta
ga 'yan'uwansa."
26 Ya kuma ce,

"Albarka ta tabbata ga UBANGIJI Allah na Shem!
Bari Kan'ana yă zama bawan Shem.
27 Allah yă ƙara fāɗin ƙasar Yafet;
bari Yafet yă zauna a tentunan Shem,
bari kuma Kan'ana yă zama bawansa."
28 Bayan ambaliyar, Nuhu ya yi shekaru 350. 29 Gaba ɗaya dai, Nuhu ya yi shekara
950, sa'an nan ya mutu.

# 10

*Tsarin Al'ummai*

1 Wannan shi ne labarin Shem, Ham da Yafet, 'ya'yan Nuhu maza, waɗanda su ma sun haifi 'ya'ya maza bayan ambaliyar.

*Mutanen Yafet*

2 'Ya'yan* Yafet maza su ne,
Gomer, Magog, Madai da Yaban, Tubal, Meshek, da kuma Tiras.
3 'Ya'yan Gomer maza su ne,
Ashkenaz, Rifat, da Togarma.
4 'Ya'yan maza Yaban su ne,
Elisha, Tarshish, Kittim da Rodanim. 5 (Daga waɗannan mutane ne masu zama a bakin teku suka bazu zuwa cikin ƙasashensu da kuma cikin al'ummansu, kowanne da yarensa.)

*Mutanen Ham*

6 'Ya'yan Ham maza su ne,
Kush, Masar, Fut, da Kan'ana.
7 'Ya'yan Kush maza su ne,
Seba, Hawila, Sabta, Ra'ama da Sabteka.
'Ya'yan Ra'ama maza kuwa su ne,
Sheba da Dedan.
8 Kush shi ne mahaifin Nimrod wanda ya yi girma ya zama jarumin yaƙi
a duniya. 9 Shi babban maharbi ne a gaban UBANGIJI. Shi ya sa akan ce,
kamar Nimrod babban maharbi a gaban UBANGIJI. 10 Cibiyoyin mulkinsa na
farko su ne Babilon, Erek, Akkad, da Kalne a cikin Shinar. 11 Daga wannan
ƙasa, sai ya tafi Assuriya, inda ya gina Ninebe, Rehobot Ir, Kala 12 da Resen,
wadda take tsakanin Ninebe da Kala; wanda yake babban birni.
13 Mizrayim shi ne mahaifin
Ludiyawa, Anamawa, Lehabiyawa, Naftuhiyawa, 14 Fetrusiyawa, da Kasluhiyawa
(inda Filistiyawa suka fito) da kuma Kaftorawa.
15 Kan'ana shi ne mahaifin,
Sidon ɗan farinsa, da na Hittiyawa, 16 Yebusiyawa, Amoriyawa, Girgashiyawa,
17 Hiwiyawa, Arkiyawa, Siniyawa, 18 Arbadiyawa, Zemarawa, da Hamawa.
Daga baya zuriyar Kan'aniyawa suka yaɗu 19 har iyakar Kan'ana ta kai Sidon ta wajen Gerar har zuwa Gaza, sa'an nan ta milla zuwa Sodom, Gomorra, Adma da Zeboyim, har zuwa Lasha.
20 Waɗannan su ne 'ya'yan Ham maza bisa ga zuriyarsu da yarurrukansu, cikin ƙasashensu da kuma al'ummominsu.

*Mutanen Shem*

* **10:2** 'Ya'ya maza na iya nufin zuriyoyi Ko kuwa magāda ko al'ummai; haka ma a ayoyi 3, 4, 6, 7, 20-23, 29 da 31.

21 Aka kuma haifa wa Shem, wan Yafet, ʼyaʼya maza. Shem shi ne kakan ʼyaʼyan Eber duka.
22 ʼYaʼyan Shem maza su ne,
Elam, Asshur, Arfakshad, Lud da Aram.
23 ʼYaʼyan Aram maza su ne,
Uz, Hul, Geter da Mash.
24 Arfakshad ne mahaifin† Shela.
Shela kuma shi ne mahaifin Eber.
25 Aka haifa wa Eber ʼyaʼya maza biyu.
Aka ba wa ɗaya suna Feleg,‡ gama a zamaninsa ne aka raba duniya; aka kuma sa wa ɗanʼuwansa suna Yoktan.
26 Yoktan shi ne mahaifin,
Almodad, Shelef, Hazarmawet, Yera, 27 Hadoram, Uzal, Dikla, 28 Obal, Abimayel,
Sheba, 29 Ofir, Hawila da Yobab. Dukan waɗannan ʼyaʼyan Yoktan maza ne.
30 Yankin da suka zauna ya miƙe daga Mesha zuwa wajen Sefar a gabashin ƙasar tudu.
31 Waɗannan su ne ʼyaʼyan Shem maza bisa ga zuriyarsu da yarurrukansu, cikin ƙasashensu da kuma alʼummominsu.

32 Waɗannan su ne zuriyar ʼyaʼyan Nuhu maza bisa ga jerin zuriyarsu cikin alʼummominsu. Daga waɗannan ne alʼummomi suka bazu koʼina a duniya bayan ambaliya.

# 11

### *Hasumiyar Babilon*

1 To, a lokacin, yaren mutanen duniya ɗaya ne, maganarsu kuma ɗaya ce. 2 Yayinda
mutane suke ta yin ƙaura zuwa gabas, sai suka sami fili a Shinar, suka zauna a can.
3 Suka ce wa juna, “Ku zo, mu yi tubula, mu gasa su sosai.” Suka yi amfani da
tubula a maimakon duwatsu, kwalta kuma a maimakon laka. 4 Saʼan nan suka ce,
“Ku zo, mu gina wa kanmu birni da hasumiyar da za tă kai har sammai, domin mu
yi wa kanmu suna, don kada mu warwatsu koʼina a doron ƙasa.”
5 Sai UBANGIJI ya sauko don yă ga birni da kuma hasumiyar da mutanen suke gini.
6 UBANGIJI ya ce, “Ga su, su jamaʼa ɗaya ce, su duka kuwa harshensu guda ne. Wannan
kuwa masomi ne kawai na abin da za su iya yi, babu kuma abin da suka yi shirya yi
da ba za su iya yi ba. 7 Zo, mu sauka, mu rikitar da harshensu don kada su fahimci
juna.”
8 Saboda haka UBANGIJI ya watsar da su daga wurin zuwa koʼina a doron ƙasa, suka
kuwa daina gina birnin. 9 Shi ya sa aka kira birnin Babel,* domin a can ne UBANGIJI
ya rikitar da harshen dukan duniya. Daga can UBANGIJI ya watsar da su koʼina a
doron ƙasa.

### *Daga Shem zuwa Abram*

10 Wannan shi ne labarin Shem.

Shekara biyu bayan ambaliya, saʼad da Shem ya yi shekara 100, sai ya haifi Arfakshad. 11 Bayan ya haifi Arfakshad, Shem ya yi shekara 500, ya haifi waɗansu ʼyaʼya maza da mata.

† **10:24** Da Ibraniyanci; Seftuwajin, mahaifin shi ne Kainan, Kainan kuwa shi ne mahaifin ‡ **10:25** Feleg yana nufin rarrabuwa. * **11:9** Wato, Babilon; Babel ya yi kamar Ibraniyanci na rikitar.

12 Sa’ad da Arfakshad ya yi shekara 35, sai ya haifi Shela. 13 Bayan ya haifi Shela
kuwa, Arfakshad ya yi shekara 403, ya kuma haifi waɗansu ’ya’ya maza da mata.[†]
14 Sa’ad da Shela ya yi shekaru 30, sai ya haifi Eber. 15 Bayan ya haifi Eber, Shela
ya yi shekara 403, ya kuma haifi waɗansu ’ya’ya maza da mata.
16 Sa’ad da Eber ya yi shekaru 34, sai ya haifi Feleg. 17 Bayan ya haifi Feleg, Eber
ya yi shekara 430, ya kuma haifi waɗansu ’ya’ya maza da mata.
18 Sa’ad da Feleg ya yi shekaru 30, sai ya haifi Reyu. 19 Bayan ya haifi Reyu, Feleg
ya yi shekara 209, ya kuma haifi waɗansu ’ya’ya maza da mata.
20 Sa’ad da Reyu ya yi shekaru 32, sai ya haifi Serug. 21 Bayan ya haifi Serug, Reyu
ya yi shekara 207, ya kuma haifi waɗansu ’ya’ya maza da mata.
22 Sa’ad da Serug ya yi shekaru 30, sai ya haifi Nahor. 23 Bayan ya haifi Nahor, Serug
ya yi shekara 200, ya kuma haifi waɗansu ’ya’ya maza da mata.
24 Sa’ad da Nahor ya yi shekaru 29, sai ya haifi Tera. 25 Bayan ya haifi Tera, Nahor
ya yi shekara 119, ya kuma haifi waɗansu ’ya’ya maza da mata.
26 Bayan Tera ya yi shekaru 70, sai ya haifi Abram, Nahor da Haran.

27 Wannan ita ce zuriyar Tera.

Tera ya haifi Abram, Nahor da Haran. Haran kuma ya haifi Lot. 28 Yayinda
mahaifinsa Tera yana da rai, Haran ya rasu a Ur ta Kaldiyawa, a ƙasar haihuwarsa.
29 Abram da Nahor suka yi aure. Sunan matar Abram, Saira ne, sunan matar Nahor
kuwa Milka; ita ’yar Haran ce, mahaifin Milka da Iska. 30 Saira kuwa bakararriya ce,
ba ta da yara.
31 Tera ya ɗauki ɗansa Abraham, jikansa Lot ɗan Haran, da surukarsa Saira, matar
Abram, tare kuwa suka bar Ur ta Kaldiyawa, don su tafi Kan’ana. Amma sa’ad da
suka zo Haran sai suka zauna a can.
32 Tera yi shekaru 205, ya kuma mutu a Haran.

# 12

*Kiran Abram*

1 Ubangiji ya ce wa Abram, “Tashi ka bar ƙasarka, da mutanenka, da iyalin
mahaifinka, ka tafi ƙasar da zan nuna maka.
2 “Zan mai da kai al’umma mai girma,
zan kuma albarkace ka;
zan sa sunanka yǎ zama mai girma,
ka kuma zama sanadin albarka.
3 Zan albarkaci duk wanda ya albarkace ka,
in kuma la’anci duk wanda ya la’anta ka,
dukan mutanen duniya
za su sami albarka ta wurinka.”
4 Saboda haka Abram ya tashi yadda Ubangiji ya faɗa masa; Lot ma ya tafi tare
da shi. Abram yana da shekaru 75, sa’ad da ya tashi daga Haran. 5 Abram ya ɗauki
matarsa Saira da Lot ɗan ɗan’uwansa, da dukan mallakar da suka tattara, da kuma
mutanen da suka samu a Haran, suka kama hanya zuwa ƙasar Kan’ana.
6 Abram ya ratsa ƙasar har zuwa wurin babban itace na More a Shekem. A lokacin
Kan’aniyawa suna a ƙasar. 7 Ubangiji ya bayyana ga Abram ya ce, “Ga zuriyarka

[†] **11:13** Da Ibraniyanci; Seftuwajin (dubi kuma Luk 3.35,36 da kuma sharhi a Far 10.24) shekaru 35, ya haifi Kainan. 13 bayan kuma ya haifi Kaina, Arfakshad ya yi shekaru 430 ya kuma haifi waɗansu ’ya’ya maza da mata, sa’an nan ya mutu. Sa’ad da Kaina ya yi shekaru ɗari da talatin, ya haifi Shela. Bayan ya haifi Shela, Kaina ya yi shekaru 330 ya kuma haifi waɗansu ’ya’ya maza da mata

ne zan ba da wannan ƙasa.” Saboda haka Abram ya gina bagade a can ga UBANGIJI, wanda ya bayyana gare shi.

[8] Daga can, ya ci gaba zuwa wajen tuddai a gabashin Betel ya kafa tentinsa, Betel yana yamma, Ai, kuma a gabas. A can ya gina bagade ga UBANGIJI ya kuma kira bisa sunan UBANGIJI.

[9] Sa’an nan Abram ya tashi ya ci gaba da tafiya zuwa wajen Negeb.

*Abram a Masar*

[10] To, a lokacin, an yi yunwa a ƙasar, sai Abram ya gangara zuwa Masar don yă
zauna a can na ɗan lokaci, domin yunwa ta yi tsanani. [11] Yayinda yana gab da shiga
Masar, sai ya ce wa matarsa Saira, “Na sani ke kyakkyawar mace ce. [12] Sa’ad da
Masarawa suka ganki, za su ce, ‘Wannan matarsa ce.’ Za su kuwa kashe ni, su bar
ki da rai. [13] Saboda haka ki ce ke ’yar’uwata ce, domin ta dalilinki a mutunta ni, a
kuma bar ni da rai.”

[14] Sa’ad da Abram ya isa Masar, Masarawa suka ga cewa Saira kyakkyawa mace
ce ƙwarai. [15] Sa’ad da fadawan Fir’auna suka gan ta kuwa, sai suka yabe ta wajen
Fir’auna, aka kuwa kawo ta cikin fadarsa. [16] Ya mutunta Abram sosai saboda ita,
Abram kuwa ya mallaki tumaki da shanu, da jakuna maza da mata, da bayi maza da
mata, da kuma raƙuma.

[17] Amma UBANGIJI ya wahalar da Fir’auna da gidansa da cututtuka masu zafi saboda
Saira, matar Abram. [18] Saboda haka Fir’auna ya kira Abram ya ce, “Me ke nan ka
yi mini? Me ya sa ba ka faɗa mini cewa ita matarka ce ba? [19] Don me ka ruɗe ni
cewa, ‘Ita ’yar’uwata ce,’ har na ɗauke ta tă zama matata? To, ga matarka. Ɗauke ta
ka tafi.” [20] Sa’an nan Fir’auna ya yi wa mutanensa umarni a kan Abram, suka kuwa
sallame shi tare da matarsa da kuma dukan abin da yake da shi.

# 13

*Abram da Lot sun rabu*

[1] Saboda haka Abram ya haura daga Masar zuwa Negeb tare da matarsa, da dukan
abin da yake da shi tare da Lot. [2] Abram ya azurta ƙwarai da dabbobi, da azurfa, da
kuma zinariya.

[3] Daga Negeb, ya ci gaba da tafiyarsa a wurare dabam-dabam har ya kai tsakanin
Betel da Ai, a inda dā ya kafa tentinsa na fari [4] da kuma inda dā ya gina bagade. A
can Abram ya kira bisa sunan UBANGIJI.

[5] Lot wanda yake tafiya tare da Abram, shi ma yana da garken shanu da tumaki da
kuma tentuna. [6] Wannan ya sa har ƙasar ba tă ishe su yayinda suke zama tare ba,
saboda mallakarsu ta yi yawa har ba za su iya zama tare ba. [7] Rikici kuma ya tashi
tsakanin masu kiwon dabbobin Abram da na Lot. Mazaunan ƙasar, a lokacin kuwa
Kan’aniyawa da Ferizziyawa ne.

[8] Saboda haka Abram ya ce wa Lot, “Kada mu bar rikici yă shiga tsakaninmu, ko
kuma tsakanin masu kiwon dabbobinka da nawa, gama mu ’yan’uwa ne. [9] Ba ga
dukan ƙasar tana gabanka ba? Bari mu rabu. In ka yi hagu sai ni in yi dama. In ka
yi dama, sai ni in yi hagu.”

[10] Lot ya ɗaga idanunsa sama ya dubi kwarin Urdun, sai ya ga kwarin yana da
ciyawa mai kyau ƙwarai sai ka ce lambun UBANGIJI, kamar ƙasar Masar, wajajen
Zowar. (Wannan fa kafin UBANGIJI yă hallaka Sodom da Gomorra.) [11] Saboda haka
sai Lot ya zaɓar wa kansa dukan kwarin Urdun, ya tashi ya nufi wajen gabas. Haka
fa suka rabu da juna. [12] Abram ya zauna a ƙasar Kan’ana, yayinda Lot ya zauna cikin
biranen kwari, ya kafa tentunansa kusa da Sodom. [13] Mutanen Sodom kuwa mugaye
ne, sun aikata zunubi ƙwarai ga UBANGIJI.

14 Bayan Lot ya rabu da Abram, sai UBANGIJI ya ce wa Abram, “Daga idanunka daga
inda kake, ka dubi arewa da kudu, gabas da yamma. 15 Dukan ƙasar da kake gani
zan ba ka, kai da zuriyarka har abada. 16 Zan sa zuriyarka tă yi yawa kamar ƙurar
ƙasa, har in wani yana iya ƙidaya ƙurar, to, za a iya ƙidaya zuriyarka. 17 Tafi, ka
ratsa tsawo da fāɗin ƙasar, gama zan ba ka ita.”
18 Saboda haka Abram ya cire tentunansa, ya zo ya zauna kusa da manyan itatuwan
Mamre a Hebron, inda ya gina bagade ga UBANGIJI.

# 14

### *Abram ya kuɓutar da Lot*

1 A zamanin Amrafel sarkin Shinar,[*] shi da Ariyok sarkin Ellasar, Kedorlayomer
sarkin Elam, da kuma Tidal sarkin Goyim 2 suka tafi don su yaƙi Bera sarkin
Sodom, Birsha sarkin Gomorra, Shinab sarkin Adma, Shemeber sarkin Zeboyim, da
kuma sarkin Bela (wato, Zowar). 3 Dukan waɗannan sarakuna na bayan nan suka
haɗa kai a Kwarin Siddim (Teku Gishiri). 4 Shekara goma sha biyu suna bauta wa
Kedorlayomer, amma a shekara ta sha uku sai suka yi tawaye.
5 A shekara ta goma sha huɗu, Kedorlayomer da sarakunan da suka haɗa kai da
shi suka tafi suka cinye Refahiyawa a Ashterot Karnayim, Zuziyawa a Ham, Emawa
a Shabe Kiriyatayim, 6 da Horiyawa a ƙasar tudun Seyir har zuwa El Faran kusa da
hamada. 7 Sa’an nan suka juya suka tafi En Mishfat (wato, Kadesh), suka cinye dukan
ƙasar Amalekawa, da kuma Amoriyawa waɗanda suke zaune a Hazazon Tamar.
8 Sai sarkin Sodom, sarkin Gomorra, sarkin Adma, sarkin Zeboyim da sarkin Bela
(wato, Zowar), suka fita suka ja dāgā a Kwarin Siddim 9 gāba da Kedorlayomer sarkin
Elam, Tidal sarkin Goyim, Amrafel sarkin Shinar da Ariyok sarkin Ellasar; sarakuna
huɗu gāba da biyar. 10 Kwarin Siddim kuwa ya cika da ramummukan kwalta, sa’ad
da sarakunan Sodom da Gomorra suka gudu kuwa, waɗansu mutane suka fāɗa cikin
ramummukan kwaltan, sauran kuwa suka gudu zuwa tuddai. 11 Sarakunan nan huɗu
suka washe dukan kayayyakin Sodom da Gomorra, da kuma dukan abincinsu, sa’an
nan suka tafi. 12 Suka kuma kama Lot ɗan ɗan’uwan Abram, wanda yake zaune a
Sodom, da kayayyakinsa, suka yi tafiyarsu.
13 Sai wani wanda ya tsira, ya zo ya faɗa wa Abram mutumin Ibraniyawa. Abram
kuwa yana zama kusa da manyan itatuwan Mamre, Mamre mutumin Amoriyawa
ne ɗan’uwan Eshkol da Aner, su kuwa abokan Abram ne. 14 Da Abram ya ji cewa
an kama danginsa, sai ya tara horarrun mutane 318, da aka haifa a gidansa, ya bi
sawun sarakunan da suka tafi da Lot, har Dan. 15 Da dad dare, Abram ya rarraba
mutanensa don su fāɗa wa sarakunan nan, ya ɗibge su, ya kore su har zuwa Hoba,
arewa da Damaskus. 16 Ya washe su da kuma dukan kayayyakinsu, ya kuma dawo
da Lot danginsa da mallakarsa, tare da mata da sauran mutane.
17 Bayan Abram ya dawo daga cin Kedorlayomer da sarakunan da suka haɗa kai
da shi a yaƙi, sai sarkin Sodom ya fito don yă tarye Abram a Kwarin Shabe (wato,
Kwarin Sarki).
18 Sai Melkizedek sarkin Salem[†] ya kawo burodi da ruwan inabi. Shi firist ne na
Allah Mafi Ɗaukaka, 19 ya albarkaci Abram yana cewa,
“Allah Mafi Ɗaukaka Mahaliccin sama da ƙasa
yă albarkace Abram.
20 Kuma albarka ta tabbata ga Allah Mafi Ɗaukaka
wanda ya ba da maƙiyanka a hannunka.”
Sa’an nan Abram ya ba shi kashi ɗaya bisa goma na kome.

[*] **14:1** Wato, Babilon; haka ma a aya 9 [†] **14:18** Wato, Urushalima

21 Sarkin Sodom ya ce wa Abram, “Ka ba ni mutanena da ka ƙwace daga hannun
sarakunan nan kawai, ka riƙe kayayyakin don kanka.”
22 Amma Abram ya ce, wa sarkin Sodom, “Na ɗaga hannu ga Ubangiji Allah Mafi
Ɗaukaka, Mahaliccin sama da ƙasa, na riga na rantse 23 cewa ba zan karɓi kome
da yake naka ba, ko zare ko maɗaurin takalma, don kada ka ce, ‘Na azurta Abram.’
24 Ba zan karɓi kome ba, sai dai abin da mutanena suka ci da kuma rabon mutanen
da suka tafi tare da ni, ga Aner, Eshkol, da Mamre. Bari su ɗauki rabonsu.”

# 15

*Alkawarin Allah da Abram*

1 Bayan wannan, maganar Ubangiji ta zo wa Abram cikin mafarki cewa,
“Kada ka ji tsoro, Abram.
Ni ne garkuwarka,
kuma ladanka zai zama mai girma.”
2 Amma Abram ya ce, “Ya Ubangiji Mai Iko Duka, mene ne za ka ba ni, ganin
cewa ba na haihuwa, wanda kuma zai gāji gādon gidana shi ne Eliyezer mutumin
Damaskus?” 3 Abram ya kuma ce, “Ga shi ba ka ba ni ɗa ba, don haka bawan da aka
haifa a gidana ne zai zama magājina.”
4 Sa’an nan maganar Ubangiji ta zo gare shi cewa, “Wannan mutum ba zai zama
magājinka ba, ɗa da yake zuwa daga jikinka ne zai zama magājinka.” 5 Sai Ubangiji
ya fito da kai shi waje ya ce, “Ka dubi sammai ka kuma ƙirga taurari, in har za ka
iya ƙirga su.” Sa’an nan ya ce masa, “Haka zuriyarka za tă zama.”
6 Abram ya gaskata, Ubangiji kuma ya lasafta shi adalci ga Abram.
7 Ubangiji ya kuma ce wa Abram, “Ni ne Ubangiji wanda ya fitar da kai daga Ur
na Kaldiyawa, domin in ba ka wannan ƙasa ka mallake ta.”
8 Amma Abram ya ce, “Ya Ubangiji Mai Iko Duka, yaya zan san cewa zan mallake
ta?”
9 Saboda haka Allah ya ce masa, “Kawo mini karsana, akuya, da kuma rago
kowanne yă kasance shi shekara uku ne, da kurciya da kuma ɗan tattabara.”
10 Abram ya kawo waɗannan duka a gaban Allah, ya raba kowannensu a tsakiya,
ya ajiye su gab da juna, amma bai tsaga tsuntsayen a tsaka ba. 11 Sai tsuntsaye masu
cin nama suka sauko a kan gawawwakin, amma Abram ya kore su.
12 Yayinda rana tana fāɗuwa, sai Abram ya yi barci mai zurfi, sai wani duhu mai
kauri mai kuma bantsoro ya rufe shi.
13 Sa’an nan Ubangiji ya ce wa Abram, “Ka sani tabbatacce cewa shekaru ɗari
huɗu, zuriyarka za tă zama baƙi a ƙasar da ba tasu ba, za a mai da su bayi, a
kuma wulaƙanta su. 14 Amma zan hukunta al’ummar da suka yi bauta kamar bayi,
daga baya kuma za su fita da mallaka mai yawa. 15 Amma kai za ka koma wurin
kakanninka cikin salama a kuma binne ka da kyakkyawan tsufa. 16 A tsara ta huɗu
zuriyarka za tă komo nan, saboda zunubin Amoriyawa bai riga ya cika ba.”
17 Sa’ad da rana ta fāɗi, aka kuwa yi duhu, sai wata tukunya mai hayaƙi,
mai harshen wuta mai ci, ta bayyana, ta kuma wuce tsakanin abubuwan nan
da aka tsaga. 18 A wannan rana, Ubangiji ya yi alkawari da Abram ya ce, “Ga
zuriyarka na ba da wannan ƙasa, daga kogin Masar zuwa babban kogi, Yuferites
ke nan, 19 ƙasar Keniyawa, Kenizziyawa, Kadmoniyawa, 20 Hittiyawa, Ferizziyawa,
Refahiyawa, 21 Amoriyawa, Kan’aniyawa, Girgashiyawa da kuma Yebusiyawa.”

# 16

*Hagar da Ishmayel*

[1] To, Saira, matar Abram, ba tă haifa masa ’ya’ya ba. Amma tana da wata baiwa
mutuniyar Masar mai suna Hagar, [2] saboda haka sai ta ce wa Abram, “UBANGIJI ya
hana mini haihuwar ’ya’ya. Tafi ka kwana da baiwata; watakila in sami iyali ta
wurinta.”

Abram kuwa ya yarda da abin da Saira ta faɗa. [3] Saboda haka bayan Abram ya
yi zama a Kan’ana shekaru goma, Saira matarsa ta ɗauki Hagar baiwarta ta ba wa
mijinta tă zama matarsa. [4] Abram kuwa ya kwana da Hagar, ta kuma yi ciki.

Sa’ad da Hagar ta gane tana da ciki, sai ta fara rena uwargijiyarta. [5] Sai Saira ta ce
wa Abram, “Kai ne da alhakin wahalan nan da nake sha. Na sa baiwata a hannunka,
yanzu da ta sani tana da ciki, sai ta fara rena ni. Bari UBANGIJI yă shari’anta tsakanina
da kai.”

[6] Abram ya ce, “Baiwarki tana a hannunki? Ki yi da ita yadda kika ga ya fi kyau.”
Sai Saira ta wulaƙanta Hagar; saboda haka ta gudu daga gare ta.

[7] Mala’ikan UBANGIJI ya sami Hagar kusa da maɓulɓula a jeji, ita ce maɓulɓular da
take gefen hanya zuwa Shur. [8] Ya kuma ce mata, “Hagar, baiwar Saira, daga ina kika
fito, kuma ina za ki?”

Ta amsa ta ce, “Ina gudu ne daga wurin uwargijiyata Saira.”

[9] Sai mala’ikan UBANGIJI ya ce mata, “Koma wurin uwargijiyarki Saira, ki yi mata
biyayya.” [10] Mala’ikan ya ƙara da cewa, “Zan ƙara zuriyarki har su yi yawan da ba
wanda zai iya lasafta su.”

[11] Mala’ikan UBANGIJI ya kuma ce mata,

“Ga shi kina da ciki
    za ki kuwa haifi ɗa.
Za ki ba shi suna Ishmayel,*
    gama UBANGIJI ya ga wahalarki.
[12] Zai zama mutum mai halin jakin jeji.
    Hannunsa zai yi gāba da kowa,
    hannun kowa kuma zai yi gāba da shi.
Zai yi zama gāba
    ga dukan ’yan’uwansa.”

[13] Sai ta ba wa UBANGIJI wanda ya yi magana da ita, wannan suna. “Kai Allah ne
wanda yake ganina,” gama ta ce, “Yanzu na ga wanda yake ganina.” [14] Shi ya sa ake
kira rijiyar Beyer-Lahai-Royi† tana nan har yanzu, tsakanin Kadesh da Bered.

[15] Haka fa Hagar ta haifa wa Abram ɗa, Abram kuwa ya ba da suna Ishmayel ga
ɗan da ta haifa. [16] Abram yana da shekaru 86 sa’ad da Hagar ta haifa masa Ishmayel.

# 17

*Alkawarin kaciya*

[1] Sa’ad da Abram ya yi shekaru 99, sai UBANGIJI ya bayyana a gare shi ya ce, ni “Ni
ne Allah Maɗaukaki,* ka yi tafiya a gabana ka kuma zama marar abin zargi. [2] Zan
tabbatar da alkawarina tsakanina da kai, zan kuma ƙara zuriyarka ta yi yawa.”

[3] Abram ya rusuna da fuskarsa har ƙasa, Allah kuma ya ce masa, [4] “Gare ni kam,
wannan shi ne alkawarina da kai, za ka zama mahaifin al’ummai masu yawa. [5] Ba
za a ƙara kiranka Abram† ba; sunanka zai zama Ibrahim,‡ gama na mai da kai
uban al’ummai masu yawa. [6] Zan sa ka azurta sosai, zan yi al’ummai daga cikinka,
sarakuna kuma za su fito daga cikinka, [7] zan kafa alkawarina kamar madawwamin
alkawari tsakanina da kai da kuma zuriyarka bayanka har tsararraki masu zuwa, in

* **16:11** Ishmayel yana nufin Allah yana ji. † **16:14** Beyer-Lahai-Royi yana nufin rijiyar Mai Rai wanda yake ganina. * **17:1** Da Ibraniyanci El-Shaddai † **17:5** Abram yana nufin uban da aka ɗaukaka. ‡ **17:5** Ibrahim yana nufin uban mutane da yawa.

zama Allahnka da kuma Allahn zuriyarka a bayanka. 8 Dukan ƙasar Kan'ana inda
kake baƙo a yanzu, zan ba da ita a matsayin madawwamiyar mallaka gare ka da
kuma zuriyarka a bayanka, zan kuma zama Allahnsu."
9 Sa'an nan Allah ya ce wa Ibrahim. "Kai fa, sai ka kiyaye alkawarina, kai da
zuriyarka bayanka, har tsararraki masu zuwa. 10 Wannan shi ne alkawarina da kai
da kuma zuriyarka a bayanka, alkawarin da za ka kiyaye ke nan. Kowane namiji
a cikinku kuwa za a yi masa kaciya. 11 Za ku yi kaciya, za tă kuma zama alamar
alkawari tsakanina da kai. 12 Daga yanzu duk namijin da aka haifa a cikinku za
a yi masa kaciya a rana ta takwas har dukan zamananku, ko haifaffen gida ne, ko
sayayye da kuɗi daga kowane baƙo wanda ba na zuriyarku ba. 13 Ko haifaffe a
gidanka ko an sayo da kuɗi, dole a yi musu kaciya. Alkawarina cikin jikinku zai
kasance madawwamin alkawari. 14 Kowane namijin da ba a yi masa kaciya a jiki ba,
za a fid da shi daga cikin mutanensa; domin ya karya alkawarina."
15 Allah ya kuma ce wa Ibrahim, "Game da Saira matarka kuwa, ba za ka ƙara
kiranta Saira ba, sunanta zai zama Saratu. 16 Zan sa mata albarka, ban da haka ma,
zan ba ka ɗa ta wurinta, zan sa mata albarka, za tă kuwa zama mahaifiyar al'ummai;
sarakunan mutane za su fito daga gare ta."
17 Ibrahim ya rusuna da fuskarsa har ƙasa, ya yi dariya, ya ce wa kansa, "Za a
haifi ɗa wa mutum mai shekaru ɗari? Saratu za tă haifi ɗa tana da shekaru tasa'in?"
18 Ibrahim ya kuma ce wa Allah, "Me zai hana a dai bar Ishmayel kawai yă gāji
alkawarin nan da ka yi mini."
19 Sai Allah ya ce, "Duk da haka dai, matarka Saratu za tă haifi maka ɗa; za ka
kuma kira shi Ishaku.§ A kansa zan tabbatar da madawwamin alkawarina, da kuma
ga zuriyarsa da za su zo bayansa. 20 Game da Ishmayel kuwa, na ji ka. Tabbatacce
zan albarkace shi, zan sa yă azurta, zai kuma ƙaru ƙwarai. Zai zama mahaifin masu
mulki goma sha biyu, zan kuma maishe shi babban al'umma! 21 Amma dai zan kafa
alkawarina da Ishaku wanda Saratu za tă haifa maka war haka shekara mai zuwa."
22 Da ya gama magana da Ibrahim, sai Allah ya tashi daga gare shi.
23 A wannan rana, Ibrahim ya ɗauki ɗansa Ishmayel da dukan waɗanda aka haifa
cikin gidansa, da waɗanda aka sayo da kuɗinsa, ya kuwa yi wa kowane namiji a
cikin gidansa kaciya kamar yadda Allah ya faɗa masa. 24 Ibrahim yana da shekara
tasa'in da tara sa'ad da aka yi masa kaciya, 25 Ishmayel ɗansa kuma yana da shekara
goma sha uku. 26 Aka yi wa Ibrahim da ɗansa Ishmayel kaciya a rana ɗaya. 27 Aka
yi wa kowane namiji a gidan Ibrahim kaciya, da waɗanda aka haifa a gidansa, da
waɗanda aka sayo da kuɗi daga baƙo.

# 18

*Baƙi guda uku*

1 UBANGIJI ya bayyana ga Ibrahim kusa da manyan itatuwan Mamre yayinda yake
zaune a mashigin tentinsa da tsakar rana. 2 Da Ibrahim ya ɗaga ido, sai ya ga mutum
uku suna tsaye kusa da shi. Sa'ad da ya gan su, sai ya tashi nan da nan daga mashigin
tentinsa, ya tarye su, ya rusuna har ƙasa.
3 Ya ce, "Ranka yă daɗe, in na sami tagomashi daga gare ku kada ku wuce bawanku.
4 Bari a kawo ruwa ku wanke ƙafafunku, ku huta a ƙarƙashin wannan itace. 5 Bari
in samo muku wani abu ku ci don ku wartsake, sa'an nan ku ci gaba da tafiyarku;
da yake kun biyo wurin bawanku."
Suka ce, "To, sai ka yi abin da ka ce."
6 Saboda haka Ibrahim ya ruga zuwa wurin Saratu a cikin tenti ya ce, "Yi sauri, ki
shirya mudu uku na gari mai laushi, ki cuɗa shi, ki yi burodi."

§ **17:19** Ishaku yana nufin ya yi dariya.

7 Sa’an nan Ibrahim ya yi gudu zuwa garkensa, ya zaɓi ɗan maraƙi ya ba wa
bawansa, bawansa kuma ya yi sauri ya gyara shi. 8 Sa’an nan Ibrahim ya ɗauko
dambu da madara da naman ɗan maraƙin da aka gyara, ya kawo a gabansu. Yayinda
suke ci, ya tsaya a gindin itace kusa da su.
9 Sai suka ce masa, “Ina Saratu matarka?”
Ibrahim ya ce, “Tana can cikin tenti.”
10 Sa’an nan ɗayansu ya ce, “Lalle zan komo wurinka war haka shekara mai zuwa.
Saratu matarka kuwa za tă haifi ɗa.”
Saratu kuwa tana a bayansu tana ji daga mashigin tenti. 11 Ibrahim da Saratu
dai sun riga sun tsufa sosai. Saratu kuma ta wuce shekarun haihuwa. 12 Saboda
haka Saratu ta yi dariya da ta yi tunani a zuci tana cewa, “Bayan ƙarfina ya ƙare,
maigidana* kuma ya tsufa, yanzu zan sami wannan jin daɗi?”
13 Sai Ubangiji ya ce wa Ibrahim, “Me ya ba Saratu dariya har da ta ce, ‘Har zan iya
haifi ɗa duk ta tsufata yanzu?’ 14 Akwai abin zai gagari Ubangiji? Zan komo wurinka
a ƙayyadadden lokacin nan shekara mai zuwa kuma Saratu za tă haifi ɗa.”
15 Saratu ta ji tsoro, don haka sai ta yi ƙarya ta ce, “Ban yi dariya ba.”
Ya ce, “A’a, kin yi dariya.”

### *Ibrahim ya yi roƙo don Sodom*

16 Sai mutanen suka tashi suka nufi Sodom, Ibrahim kuwa ya yi musu rakiya, ya
yi bankwana da su. 17 Sai Ubangiji ya ce, “Zan ɓoye wa Ibrahim abin da nake shirin
yi? 18 Lalle Ibrahim zai zama al’umma mai girma da kuma mai iko, kuma ta wurinsa
dukan al’umman duniya za su sami albarka. 19 Saboda na zaɓe shi don yă umarci
’ya’yansa da iyalinsa a bayansa su kiyaye hanyoyin Ubangiji, ta wurin yin abin da
yake daidai da kuma yin adalci, domin Ubangiji ya aikata abin da ya yi wa Ibrahim
alkawari.”
20 Sa’an nan Ubangiji ya ce, “Kuka a kan Sodom da Gomorra ta yi yawa, zunubinsu
kuma ya yi muni sosai, 21 zan gangara in ga ko abin da suka yi ya yi muni kamar
yadda kukan ya zo gare ni, zan bincike.”
22 Sai mutanen suka juya suka nufi wajen Sodom amma Ibrahim ya ci gaba da
kasance a gaban Ubangiji.† 23 Sai Ibrahim ya matso wurinsa ya ce, “Za ka hallaka
masu adalci tare da masu mugunta? 24 Me zai faru in akwai mutum hamshin masu
adalci a cikin birnin? Ashe, za ka hallaka shi, ba za ka cece wurin saboda mutane
hamsin nan masu adalcin da suke a cikinsa ba? 25 Tabbatacce ba za ka taɓa aikata
irin wannan abu ba, ka kashe masu adalci tare da masu mugunta, ka ɗauka masu
adalci da masu mugunta daidai? Tabbatacce ba za ka taɓa aikata irin wannan abu
ba! Mai hukuncin dukan duniya ba zai aikata gaskiya ba?”
26 Ubangiji ce, “In na sami mutum hamshin masu adalci a cikin birnin Sodom, zan
bar dukan birnin saboda su.”
27 Sai Ibrahim ya ƙara cewa, “Yanzu da na yi karambani har na yi magana da
Ubangiji, ko da yake ni ba kome ba ne illa turɓaya da toka, 28 in yawan masu adalci
sun kāsa hamshin da mutum biyar fa? Za ka hallaka dukan birnin saboda rashin
mutum biyar ɗin?”
Ya ce, “In na sami mutum arba’in da biyar a wurin, ba zan hallaka shi ba.”
29 Ya sāke cewa, “In mutum arba’in kaɗai aka samu a can fa?”
Ya ce, “Saboda mutum arba’in ɗin, ba zan aikata ba.”
30 Sai ya ce, “Kada Ubangiji ya yi fushi, amma bari in ƙara magana. A ce mutum
talatin kaɗai aka samu a can fa?”
Ya ce, “Ba zan aikata ba, in na sami mutum talatin a can.”

---

* **18:12** Ko kuwa miji † **18:22** Rubuce-rubucen Masoretik; rubutacciyar al’ada ta tsohon Ibraniyanci suna da amma Ubangiji ya ci gaba da kasance a gaban Ibrahim ne a nan.

31 Ibrahim ya ce, "Yanzu fa da na yi karambani har na yi magana da Ubangiji, in
ashirin kaɗai aka samu a can fa?"
Ya ce, "Saboda ashirin ɗin, ba zan hallaka shi ba."
32 Sa'an nan Ibrahim ya ce, "Kada Ubangiji yǎ yi fushi, amma bari in ƙara magana
sau ɗaya tak. In aka sami mutum goma kaɗai a can fa?"
Ubangiji ya ce, "Saboda goma nan, ba zan hallaka shi ba."
33 Sa'ad da UBANGIJI ya gama magana da Ibrahim, ya tafi, Ibrahim kuma ya koma
gida.

# 19

*An hallaka Sodom da Gomorra*
1 Mala'ikun nan biyu suka iso Sodom da yamma. Lot kuwa yana zama a hanyar
shiga birnin. Da ya gan su, sai ya tashi don yǎ tarye su, ya kuma rusuna da fuskarsa
har ƙasa. 2 Ya ce, "Ranku yǎ daɗe, ina roƙonku ku ratsa zuwa gidan bawanku. Ku
wanke ƙafafunku, ku kwana, sa'an nan ku kama hanyarku da sassafe."
Suka ce, "A'a, za mu kwana a dandali."
3 Amma ya nace musu ƙwarai, sai suka tafi tare da shi, suka kuma shiga gidansa.
Ya shirya musu abinci, ya gasa burodi marasa yisti, suka ci. 4 Kafin suka shiga barci,
sai ga dukan mutane, ƙanana da manya daga kowane ɓangare na birnin Sodom, suka
kewaye gidan. 5 Suka kira Lot, suka ce, "Ina mutanen da suka zo wurinka a daren
nan? Fito mana da su waje domin mu kwana da su."
6 Lot ya fita daga cikin gida, ya rufe ƙofar a bayansa. Ya je wurin mutanen 7 ya
ce musu, "A'a, abokaina kada ku yi wannan mummunan abu. 8 Duba, ina da 'ya'ya
mata biyu waɗanda ba su taɓa sanin namiji ba, bari in kawo muku su ku yi kome
da kuke so da su. Amma kada ku taɓa waɗannan mutane, gama su baƙina ne kuma
dole in tsare su."
9 Sai mutanen birnin suka amsa, "Ba mu wuri! Wannan mutum ya zo nan kamar
baƙo, ga shi yanzu yana so yǎ zama alƙali! Za mu wulaƙanta ka fiye da su." Suka ci
gaba da matsa wa Lot lamba, suka matsa kusa domin su fasa ƙofar.
10 Amma mutanen da suke ciki suka miƙa hannunsu, suka ja Lot zuwa cikin gida,
suka rufe ƙofar. 11 Sai suka bugi mutanen da suke a bakin ƙofar gidan da makanta,
ƙanana da manya duka, har suka gajiyar da kansu, suna lalluba inda ƙofar take.
12 Mutanen nan biyun suka ce wa Lot, "Kana da wani a nan, ko surukai, ko 'ya'ya
maza ko mata, ko kuwa wani dai a cikin birni wanda yake naka? Ka fitar da su
daga nan, 13 gama za mu hallaka wannan wuri. Kukan da aka yi ga UBANGIJI game
da mutanen birnin nan ya yi yawa sosai, ya sa har ya aiko mu domin mu hallaka
birnin."
14 Saboda haka Lot ya tafi ya yi magana da surukansa waɗanda suka yi alkawari za
su aure 'ya'yansa mata. Ya ce, "Ku yi sauri ku fita daga wannan wuri, gama UBANGIJI
yana gab da hallaka birnin." Amma surukansa suka ɗauka wasa yake yi.
15 Gari na wayewa, sai mala'ikun nan suka ƙarfafa Lot suna cewa, "Yi sauri! Ka
ɗauki matarka da 'ya'yanka biyu mata waɗanda suke a nan, don kada a shafe ku
sa'ad da ake hukunta birnin."
16 Da yana jan jiki, sai mutanen suka kama hannunsa da hannuwan matarsa da na
'ya'yansa biyu mata, suka kai su bayan birni, gama UBANGIJI ya nuna musu jinƙai.
17 Da suka fitar da su, sai ɗaya daga cikin mala'ikun ya ce, "Ku gudu domin ranku;
kada ku duba baya, kada kuma ku tsaya ko'ina cikin kwarin! Ku gudu zuwa cikin
duwatsu, don kada a hallaka ku!"
18 Amma Lot ya ce musu, "A'a, ranka yǎ daɗe, ka yi haƙuri! 19 Bawanku ya riga
ya sami tagomashi daga gare ku, kun kuma nuna mini alheri mai yawa. Ba zan iya

in gudu zuwa duwatsu ba, wannan masifa za tă same ni, zan kuma mutu. 20 Ga ɗan
gari can ya fi kusa inda zan gudu in fake. Bari in gudu zuwa can, in tsirar da raina.”
21 Sai ya ce masa, “Na yarda da abin da ka ce, ba zan hallakar da garin da ka ambata
ba. 22 Gaggauta, ka gudu zuwa can, ba zan yi kome ba sai ka isa can.” (Domin haka
ne ake kira garin Zowar.)*
23 A lokacin da Lot ya isa Zowar, rana ta hau. 24 Sai UBANGIJI ya yi ta zuba kibiritu
a bisa Sodom da Gomorra daga sama. 25 Haka ya hallakar da waɗannan birane da
kuma kwarinsu gaba ɗaya, haɗe da dukan waɗanda suke zama a biranen, da kuma
dukan shuke-shuke da suke cikin ƙasar. 26 Amma matar Lot ta waiwaya baya, ta
kuma zama ginshiƙin gishiri.
27 Da sassafe kashegari, Ibrahim ya tashi ya koma wurin da dā ya tsaya a gaban
UBANGIJI. 28 Ya duba ta wajen Sodom da Gomorra, da wajen dukan filayen ƙasar, sai
ya ga hayaƙi baƙin ƙirin yana tashi daga ƙasar kamar hayaƙi daga matoya.
29 Saboda haka sa'ad da Allah ya hallaka waɗannan biranen kwarin, ya tuna da
Ibrahim, ya kuma fitar da Lot daga masifar da ta hallaka biranen da Lot ya zauna.

### *Asalin Mowabawa da Ammonawa*

30 Lot da 'ya'yansa biyu mata suka bar Zowar suka kuma zauna a cikin duwatsu,
gama ya ji tsoro yă zauna a Zowar. Shi da 'ya'yansa biyu mata suka zauna a ciki wani
kogo. 31 Wata rana 'yarsa babba ta ce wa ƙanuwarta, “Mahaifinmu ya tsufa, kuma
babu wani mutum kusa a nan da zai yi mana ciki mu haifi 'ya'ya; yadda al'ada take
a ko'ina a duniya. 32 Bari mu sa mahaifinmu yă sha ruwan inabi, sa'an nan sai mu
kwana da shi, don kada zuriyar mahaifinmu ta ƙare.”
33 A wannan dare, suka sa mahaifinsu ya sha ruwan inabi, 'yar farin ta shiga ta
kwana da shi. Shi kuwa bai san sa'ad da ta kwanta ko sa'ad da ta tashi ba.
34 Kashegari, 'yar farin ta ce wa ƙanuwar, “Jiya da dare na kwana da mahaifina.
Bari mu sa yă sha ruwan inabi kuma yau da dare, ke ma ki shiga ki kwana da shi,
domin kada zuriyar mahaifinmu ta ƙare.” 35 Sai suka sa mahaifinsu ya sha ruwan
inabi, a wannan dare ma, ƙanuwar ta shiga ta kwana da shi. Bai kuwa san sa'ad da
ta kwanta ko sa'ad da ta tashi ba.
36 Ta haka 'ya'yan Lot biyu mata duk suka yi ciki daga mahaifinsu. 37 'Yar farin
ta haifi ɗa, ta kuma ba shi suna Mowab, shi ne mahaifin Mowabawa a yau. 38 'Yar
ƙaramar ma ta haifi ɗa, ta kuwa ba shi suna Ben-Ammi,† shi ne mahaifin Ammonawa
a yau.

# 20

### *Ibrahim da Abimelek*

1 Daga Mamre, Ibrahim ya kama hanya ya nufi wajajen Negeb, ya zauna a tsakanin
Kadesh da Shur. Ya zauna a Gerar na ɗan lokaci, 2 a can ne Ibrahim ya ce game da
matarsa Saratu, “Ita 'yar'uwata ce.” Sai Abimelek sarkin Gerar ya aiko a kawo masa
Saratu.
3 Amma wata rana da dad dare Allah ya zo wa Abimelek a cikin mafarki ya ce
masa, “Kai da matacce ɗaya kuke, saboda matar da ka ɗauka. Ita matar aure ce.”
4 Abimelek dai bai riga ya kusace ta ba tukuna, saboda haka ya ce, “Ya Ubangiji za
ka hallaka al'umma marar laifi? 5 Ba shi ne ya ce mini, 'Ita 'yar'uwata ba ce,' ita ma
ba tă ce, 'Shi ɗan'uwana ba ne'? Na yi haka da kyakkyawan nufi da hannuwa masu
tsabta.”
6 Sai Allah ya ce masa a cikin mafarki “I, na san ka yi wannan da kyakkyawan
nufi, saboda haka ne na kiyaye ka daga yin mini zunubi. Shi ya sa ban bar ka ka
taɓa ta ba. 7 Yanzu ka komar da matar mutumin, gama shi annabi ne, zai kuma yi

* **19:22** Zowar yana nufin ƙarami. † **19:38** Ben-Ammi yana nufin ɗan mutanena.

maka addu'a, za ka kuwa rayu. In ba ka komar da ita ba fa, ka sani tabbatacce kai
da dukan abin da yake naka za ku mutu."
8 Kashegari da sassafe, sai Abimelek ya tara dukan fadawansa, ya faɗa musu duk
abin da ya faru, suka ji tsoro ƙwarai da gaske. 9 Sa'an nan Abimelek ya kira Ibrahim
ciki ya ce, "Me ke nan ka yi mana? Ta wace hanya ce na yi maka laifi har da ka kawo
irin wannan babban laifi a kaina da kuma masarautata? Ka yi mini abubuwan da
bai kamata a yi ba." 10 Abimelek ya kuma ce wa Ibrahim, "Me ya sa ka yi wannan?"
11 Ibrahim ya ce, "Na ce a raina, 'Tabbatacce babu tsoron Allah a wannan wuri, za
su kuwa kashe ni saboda matata.' 12 Ban da haka, tabbatacce ita 'yar'uwata ce, 'yar
mahaifina, ko da yake ba daga uwata ba, ta kuma zama matata. 13 Sa'ad da Allah ya
sa na tashi daga gidan mahaifina na ce mata, 'Wannan shi ne yadda za ki nuna mini
ƙaunarki. Duk inda muka tafi, ki ce game da ni, "Shi ɗan'uwana ne." ' "
14 Sai Abimelek ya kawo awaki da shanu da bayi maza da mata, ya ba wa Ibrahim,
ya kuma komar da Saratu matarsa gare shi. 15 Abimelek ya kuma ce, "Kasata tana
gabanka, ka zauna a duk inda kake so."
16 Ga Saratu kuwa ya ce, "Ina ba wa ɗan'uwanki shekel dubu na azurfa, shaida
ce ta tabbatarwa a idanun dukan waɗanda suke tare da ke, da kuma a gaban kowa
cewa ba ki da laifi."
17 Sai Ibrahim ya yi addu'a ga Allah, Allah kuma ya warkar da Abimelek, da matarsa
da bayinsa mata domin su haihu, 18 gama UBANGIJI ya rufe kowace mahaifa a gidan
Abimelek saboda Saratu, matar Ibrahim.

# 21

*Haihuwar Ishaku*

1 Ana nan sai UBANGIJI ya nuna wa Saratu alheri kamar yadda ya ce, UBANGIJI kuma
ya yi wa Saratu abin da ya yi alkawari. 2 Saratu ta yi ciki, ta kuma haifa wa Ibrahim
ɗa a tsufansa; a daidai lokacin da Allah ya yi masa alkawari. 3 Ibrahim ya sa wa ɗan
da Saratu ta haifa masa suna Ishaku. 4 Sa'ad da ɗansa Ishaku ya kai kwana takwas da
haihuwa, sai Ibrahim ya yi masa kaciya, kamar yadda Allah ya umarce shi. 5 Ibrahim
yana da shekara ɗari, sa'ad da aka haifa masa ɗansa Ishaku.
6 Saratu ta ce, "Allah ya sa na yi dariya, kuma duk wanda ya ji game da wannan,
zai yi dariya tare da ni." 7 Ta kuma ƙara da cewa, "Dā, wa zai iya ce wa Ibrahim,
Saratu za tă yi renon yara? Duk da haka na haifar masa ɗa cikin tsufansa."

*An kori Hagar da Ishmayel*

8 Yaron ya yi girma, aka kuma yaye shi, a ranar da aka yaye shi kuwa, Ibrahim ya
yi babban biki. 9 Amma Saratu ta ga cewa yaron da Hagar, mutuniyar Masar ta haifa
wa Ibrahim yana wa ɗanta Ishaku gori, 10 sai ta ce wa Ibrahim, "Ka kori baiwan nan
tare da ɗanta, saboda ɗan baiwan nan ba zai taɓa raba gādo da ɗana Ishaku ba."
11 Al'amarin ya ɓata wa Ibrahim rai sosai domin zancen ya shafi ɗansa. 12 Amma
Allah ya ce wa Ibrahim, "Kada hankalinka yă tashi game da yaron nan da kuma
baiwarka. Ka saurari duk abin da Saratu ta faɗa maka, saboda ta wurin Ishaku ne za
a lissafta zuriyarka. 13 Zan ba ɗan baiwan nan al'umma shi ma, domin shi zuriyarka
ne."
14 Kashegari da sassafe sai Ibrahim ya ɗauki abinci da salkar ruwa, ya ba wa Hagar.
Ya ɗora su a kafaɗunta, sa'an nan ya sallame ta da yaron. Ta kama hanyarta ta kuma
yi ta yawo a cikin jejin Beyersheba.
15 Sa'ad da ruwan da yake cikin salkan ya ƙare, sai ta ajiye yaron a ƙarƙashin wani
ƙaramin itace. 16 Sai ta tafi, ta zauna ɗan nesa da yaron, misalin nisan harbin baka,

gama ta yi tunani ta ce, “Ba zan iya kallon yaron yana mutuwa ba.” Da ta zauna nesa
da yaron, sai ta* fara kuka.
17 Allah kuwa ya ji yaron yana kuka, sai mala’ikan Allah ya kira Hagar daga sama
ya ce mata, “Mene ne damuwarki, Hagar? Kada ki ji tsoro, Allah ya ji yaron yana
kuka yayinda yake kwance a can. 18 Ki ɗaga yaron ki riƙe shi a hannu, gama zan mai
da shi al’umma mai girma.”
19 Sa’an nan Allah ya buɗe idanunta ta ga wata rijiyar ruwa. Don haka sai ta tafi
ta cika salkan da ruwa, ta kuma ba wa yaron ruwa ya sha.
20 Allah ya kasance da yaron, yayinda yake girma. Ya yi zama a jeji, ya kuma zama
maharbi. 21 Yayinda yake zama a Jejin Faran, sai mahaifiyarsa ta samo masa mata
daga Masar.

### *Yarjejjeniya a Beyersheba*

22 A lokacin nan Abimelek da Fikol, komandan rundunoninsa suka zo suka ce wa
Ibrahim, “Allah yana tare da kai a ko mene ne kake yi. 23 Yanzu ka rantse mini a nan
a gaban Allah cewa, ba za ka yaudare ni ko ’ya’yana ko kuma zuriyata ba. Ka nuna
mini alheri, kai da ƙasar da kake zama baƙunci kamar yadda na nuna maka.”
24 Ibrahim ya ce, “Na rantse.”
25 Sa’an nan Ibrahim ya kawo kuka ga Abimelek game da rijiyar ruwan da bayin
Abimelek suka ƙwace. 26 Sai Abimelek ya ce, “Ban san wanda ya yi wannan ba. Ba
ka faɗa mini ba, ban kuwa taɓa ji ba, sai yau.”
27 Sai Ibrahim ya kawo tumaki da shanu ya ba wa Abimelek, sai su biyun suka yi
yarjejjeniya. 28 Ibrahim ya ware ’yan raguna bakwai daga cikin garke, 29 sai Abimelek
ya ce wa Ibrahim, “Mene ne ma’anar ’yan raguna bakwai da ka keɓe?”
30 Ibrahim ya amsa ya ce, “Ka karɓi waɗannan ’yan tumaki bakwai daga hannuna
a matsayin shaida cewa ni ne na haƙa wannan rijiya.”
31 Saboda haka aka kira wurin Beyersheba, domin a nan ne su biyun suka yi
rantsuwa.
32 Bayan da aka yi yarjejjeniya a Beyersheba, sai Abimelek da Fikol, komandan
rundunoninsa suka koma ƙasar Filistiyawa. 33 Sai Ibrahim ya shuka itacen tsamiya a
Beyersheba, a can kuma ya kira bisa sunan UBANGIJI, Allah Madawwami. 34 Ibrahim
kuwa ya zauna a ƙasar Filistiyawa na dogon lokaci.

## 22

### *An gwada Ibrahim*

1 Bayan abubuwan nan suka faru, sai Allah ya gwada Ibrahim. Ya ce masa,
“Ibrahim!”
Ibrahim ya amsa ya ce, “Ga ni.”
2 Sai Allah ya ce, “Ka ɗauki ɗanka, makaɗaicin ɗanka Ishaku, wanda kake ƙauna,
ka tafi yankin Moriya, ka miƙa shi hadaya ta ƙonawa a can a kan ɗaya daga cikin
duwatsun da zan nuna maka.”
3 Kashegari da sassafe, Ibrahim ya tashi ya ɗaura wa jakinsa sirdi. Ya ɗauki bayinsa
biyu, da ɗansa Ishaku. Bayan ya faskare isashen itace saboda hadaya ta ƙonawa sai
ya kama hanya zuwa wurin da Allah ya faɗa masa. 4 A rana ta uku Ibrahim ya ɗaga
ido sai ya ga wurin daga nesa. 5 Ibrahim ya ce wa bayinsa, “Ku tsaya a nan da jakin,
ni da yaron kuwa mu haura can. Za mu yi sujada sa’an nan mu komo wurinku.”
6 Ibrahim ya ɗauki itace saboda hadaya ta ƙonawa ya ɗora wa ɗansa Ishaku, shi
kuwa ya riƙe wuƙa da wutar. Yayinda su biyun suke tafiya, 7 sai Ishaku ya yi tambaya,
ya ce wa mahaifinsa Ibrahim, “Baba?”

* **21:16** Da Ibraniyanci; Seftuwajin yaron.

Ibrahim ya ce masa, “Na’am ɗana!”
Ishaku ya ce, “Ga dai wuta, ga kuma itace, amma ina ɗan ragon hadaya ta
ƙonawa?”
8 Ibrahim ya amsa ya ce, “Ɗana, Allah kansa zai tanada ɗan ragon hadayar
ƙonawa.” Sai su biyu suka ci gaba da tafiya.
9 Sa’ad da suka isa wurin da Allah ya faɗa masa, sai Ibrahim ya gina bagade a can,
ya kuma shisshirya itacen a kai. Ya ɗaura ɗansa Ishaku, ya kwantar da shi a kan
itacen, a bisa bagaden. 10 Sa’an nan Ibrahim ya miƙa hannunsa ya ɗauki wuƙar don
yǎ yanka ɗansa. 11 Amma mala’ikan UBANGIJI ya kira shi daga sama ya ce, “Ibrahim,
Ibrahim!”
Sai Ibrahim ya amsa ya ce, “Ga ni.”
12 Mala’ikan ya ce, “Kada ka yi wa yaron nan rauni. Kada kuma ka ji masa ciwo.
Yanzu na san cewa kana tsoron Allah, gama ba ka hana ni ɗanka, makaɗaicin ɗanka
ba.”
13 Ibrahim ya ɗaga ido, ya duba, sai ya ga rago da ƙahoninsa a kafe a wani ɗan
kurmi. Sai Ibrahim ya tafi ya kamo ragon ya miƙa shi hadaya ta ƙonawa a maimakon
ɗansa. 14 Ibrahim kuwa ya ba wa wurin suna, UBANGIJI Zai Tanada. Gama kamar
yadda ake ce har yǎ zuwa yau, “A bisan dutsen UBANGIJI, za a tanada.”
15 Mala’ikan UBANGIJI ya kira Ibrahim daga sama sau na biyu 16 ya ce, “Na rantse
da kaina, in ji UBANGIJI, domin ka yi wannan, ba ka kuwa hana ni ɗanka, makaɗaicin
ɗanka ba, 17 tabbatacce zan albarkace ka, zan kuma sa zuriyarka su yi yawa kamar
taurari a sararin sama, kamar kuma yashi a bakin teku. Zuriyarka za su mallaki
biranen abokan gābansu, 18 ta wurin zuriyarka kuma dukan al’umman duniya za su
sami albarka, domin ka yi mini biyayya.”
19 Sa’an nan Ibrahim ya koma wurin bayinsa, suka kuma kama hanya tare zuwa
Beyersheba. Ibrahim kuwa ya yi zamansa a Beyersheba.

### *’Ya’yan Nahor maza*

20 Bayan wani ɗan lokaci, sai aka faɗa wa Ibrahim cewa, “Ga shi, Milka ita ma ta
haifa wa Nahor ɗan’uwanka, ’ya’ya maza;
21 ɗan fari shi ne Uz, ɗan’uwansa kuma Buz,
Kemuwel (shi ne mahaifin Aram),
22 Kesed, Hazo, Fildash; Yidlaf, da kuma Betuwel.”
23 Betuwel ya haifi Rebeka.
Milka ta haifa wa Nahor ɗan’uwan Ibrahim waɗannan ’ya’ya maza takwas.

24 Ban da haka ma, ƙwarƙwararsa, mai suna Reyuma, ta haifa masa ’ya’ya maza,
Teba, Gaham, Tahash da kuma Ma’aka.

## 23

### *Mutuwar Saratu*

1 Saratu ta yi shekara ɗari da ashirin da bakwai a duniya. 2 Ta rasu a Kiriyat Arba
(wato, Hebron) a ƙasar Kan’ana, Ibrahim kuwa ya tafi ya yi makokin Saratu, yana
kuka saboda ita.
3 Sai Ibrahim ya tashi daga gefen matarsa da ta mutu, ya yi magana da Hittiyawa.*
Ya ce, 4 “Ni baƙo ne, kuma baƙo a cikinku. Ku sayar mini da wani wuri yǎ zama
wurin binnewa a nan, domin in binne mataccena.”
5 Hittiyawa suka ce wa Ibrahim, 6 “Ranka yǎ daɗe, ka saurare mu. Kai babban
yerima ne a cikinmu. Ka binne mataccenka a kabari mafi kyau na kaburburanmu.
Babu waninmu da zai hana ka kabarinsa don binne mataccenka.”

* **23:3** Ko kuwa ’ya’yan Het maza; haka ma a ayoyi 5, 7, 10, 16, 18 da 20

7 Sai Ibrahim ya tashi ya rusuna a gaban mutanen ƙasar, wato, Hittiyawan. 8 Ya
ce musu, “In kuna so in binne mataccena, sai ku ji ni, ku roƙi Efron ɗan Zohar
a madadina 9 domin yă sayar mini da kogon Makfela, wanda yake nasa, wannan
da yake a ƙarshen filinsa. Ku ce masa yă sayar mini a cikakken farashi, yă zama
mallakata domin makabarta tsakaninku.”
10 Efron mutumin Hitti yana zaune a cikin mutanensa, sai ya amsa wa Ibrahim a
kunnuwan dukan Hittiyawa waɗanda suka zo ƙofar birni. 11 Ya ce, “A’a, ranka yă
daɗe, ka ji ni, na ba ka filin, na kuma ba ka kogon da yake cikinsa. Na ba ka shi a
gaban mutanena. Ka binne mataccenka.”
12 Ibrahim ya sāke rusuna a gaban mutanen ƙasar 13 ya ce wa Efron a kunnuwansu,
“Ka ji, in ka yarda. Zan biya farashin filin. Ka karɓa daga gare ni don in iya binne
mataccena a can.”
14 Efron ya ce wa Ibrahim, 15 “Ka saurare ni, ranka yă daɗe; darajan filin ya kai
shekel ɗari huɗu na azurfa, amma mene ne wannan a tsakanina da kai? Ka binne
mataccenka.”
16 Ibrahim ya yarda da sharuɗan Efron, sai ya auna masa farashin da ya faɗa a
kunnuwan Hittiyawa, shekel ɗari huɗu na azurfa, bisa ga ma’aunin da ’yan kasuwa
suke amfani da shi a lokacin.
17 Ta haka filin Efron a Makfela kusa da Mamre, wato, filin da kogon a cikinsa, da
kuma dukan itatuwan da suke cikin iyakoki filin, aka 18 ba wa Ibrahim a matsayin
mallakarsa a gaban dukan Hittiyawa waɗanda suka zo ƙofar birnin. 19 Bayan wannan
Ibrahim ya binne matarsa Saratu a kogon a filin Makfela kusa da Mamre (wanda yake
a Hebron) a ƙasar Kan’ana. 20 Da filin da kuma kogon da yake cikinsa, Hittiyawa suka
tabbatar wa Ibrahim a matsayin makabarta.

# 24

*Ishaku da Rebeka*
1 Yanzu fa Ibrahim ya tsufa, yana da shekaru masu yawa, Ubangiji kuma ya
albarkace shi a kowace hanya. 2 Sai Ibrahim ya ce wa babban bawan gidansa, wanda
yake lura da duk abin da yake da shi, “Sa hannunka a ƙarƙashin cinyata. 3 Ina so ka
rantse da sunan Ubangiji Allah na sama da ƙasa, cewa ba za ka samo wa ɗana mata
daga ’yan matan Kan’aniyawa, waɗanda nake zama cikinsu ba. 4 Amma za ka tafi
ƙasata da kuma cikin ’yan’uwana, ka samo mata saboda ɗana Ishaku.”
5 Bawan ya ce masa, “Me zai faru in matar ba tă yarda tă zo tare da ni zuwa wannan
ƙasa ba? In komar da ɗanka a ƙasar da ka fito ne ke nan?”
6 Ibrahim ya ce, “Ka tabbata ba ka komar da ɗana can ba.” 7 Ubangiji Allah na
sama, wanda ya fitar da ni daga gidan mahaifina, da kuma ƙasar asalina wanda
kuma ya yi magana da ni, ya yi mini alkawari da rantsuwa cewa, “Ga zuriyarka zan
ba da wannan ƙasa, zai aika mala’ikansa yă sha gabanka domin ka samo wa ɗana
mata daga can. 8 In matar ba tă yarda tă zo tare da kai ba, za a kuɓutar da kai daga
wannan rantsuwa. Sai dai kada ka kai ɗana a can.” 9 Saboda haka bawan ya sa
hannunsa a ƙarƙashin cinyar maigidansa Ibrahim, ya kuma rantse masa game da
wannan al’amari.
10 Sai bawan ya ɗibi raƙuma goma na maigidansa ya tafi, ɗauke da kowane irin
abubuwa masu kyau daga wurin maigidansa. Ya fita don yă tafi Aram-Naharayim,
ya kama hanyarsa zuwa garin Nahor. 11 Ya sa raƙuman suka durƙusa kusa da rijiya
a bayan gari; wajen yamma ne, lokacin da mata sukan fita ɗiban ruwa.
12 Sai ya yi addu’a ya ce, “Ya Ubangiji Allah na maigidana Ibrahim, ka ba ni nasara
yau, ka kuma nuna alheri ga maigidana Ibrahim. 13 Duba, ina tsaye a bakin rijiyar
ruwa, ’ya’ya matan mutanen gari kuma suna fitowa domin ɗiban ruwa. 14 Bari yă
zama sa’ad da na ce wa wata yarinya, ‘Ina roƙonki ki saukar da tulunki domin in

sha,’ in ta ce, ‘Ka sha, zan kuma ba wa raƙumanka ma’; bari tă zama ita ce ka zaɓa
wa bawanka Ishaku. Ta haka zan san cewa ka nuna wa maigidana alheri.”

15 Kafin ya gama addu’a, sai Rebeka ta fito da tulu a kafaɗarta. Ita ’yar Betuwel ɗan
Milka, matar Nahor, ɗan’uwan Ibrahim. 16 Yarinyar kuwa kyakkyawa ce, budurwa,
ba namijin da ya taɓa kwana da ita. Ta gangara zuwa rijiyar, ta cika tulunta ta kuma
hauro.

17 Bawan ya yi sauri ya same ta ya ce, “Ina roƙonki ki ba ni ɗan ruwa daga tulunki.”

18 Ta ce, “Ka sha, ranka yă daɗe,” ta yi sauri ta saukar da tulun a hannuwanta, ta
kuma ba shi, ya sha.

19 Bayan ta ba shi ya sha, sai ta ce, “Zan ɗebo wa raƙumanka ruwa su ma, har sai
sun gama sha.” 20 Sai ta yi sauri ta juye ruwan da yake tulunta cikin kwami, ta koma
zuwa rijiyar da gudu don ta ƙara ɗebo ruwa, ta kuma ɗebo isashe saboda dukan
raƙumansa. 21 Mutumin bai ce uffam ba, ya dai kalle ta sosai don yă san ko Ubangiji
ya ba shi nasara a tafiyarsa ko babu.

22 Sa’ad da raƙuman suka gama shan ruwa, mutumin ya fitar da zoben hanci na
zinariya mai nauyin giram biyar da warwaro biyu na zinariya masu nauyin shekel
goma, ya ba ta. 23 Sa’an nan ya tambaye ta ya ce, “Ke ’yar wace ce? Ina roƙonki ki
faɗa mini, akwai wuri a gidan mahaifinki da za mu kwana?”

24 Sai ta ce masa, “Ni ’yar Betuwel ce ɗan da Milka ta haifa wa Nahor.” 25 Ta ƙara
da cewa, “Muna da isashen ciyawa da abincin dabbobi, da kuma wuri domin ku
kwana.”

26 Sa’an nan mutumin ya rusuna ya yi wa Ubangiji sujada, 27 yana cewa, “Yabo
ya tabbata ga Ubangiji Allah na maigidana Ibrahim, wanda bai daina nuna alheri
da amincinsa ga maigidana ba. Ni kam, Ubangiji ya bishe ni a tafiyata zuwa gidan
’yan’uwan maigidana.”

28 Yariyan ta gudu ta faɗa wa mutanen gidan mahaifiyarta game da abubuwan
nan. 29 Rebeka fa tana da wani ɗan’uwa mai suna Laban, sai ya yi hanzari ya fita
zuwa wurin mutumin a rijiyar. 30 Nan da nan da ya ga zoben hancin da warwaro a
hannuwan ’yar’uwansa, ya kuma ji Rebeka ta faɗa abin da mutumin ya ce mata, sai
ya fita zuwa wurin mutumin, ya same shi yana tsaye wajen raƙuma kusa da rijiyar.
31 Sai ya ce, “Zo, ya kai mai albarka na Ubangiji, don me kake tsaye a waje? Gama
na shirya gida da wuri domin raƙuma.”

32 Don haka mutumin ya tafi gidan, aka kuma saukar da kaya kan raƙuman. Aka
kawo wa raƙuman ciyawa da abincin dabbobi, aka kuma kawo ruwa dominsa da
mutanensa su wanke ƙafafunsu. 33 Sa’an nan aka ajiye abinci a gabansa, amma ya
ce, “Ba zan ci ba, sai na faɗi abin da yake tafe da ni.”

Sai Laban ya ce, “Faɗa mana.”

34 Saboda haka ya ce, “Ni bawan Ibrahim ne. 35 Ubangiji ya albarkaci maigidana
sosai, ya kuma zama mai arziki. Ya ba shi tumaki, shanu, azurfa, zinariya, bayi maza
da mata, raƙuma, da kuma jakuna. 36 Saratu matar maigidana ta haifa masa ɗa a
tsufanta, ya kuma ba shi duk mallakarsa. 37 Maigidana ya sa na yi rantsuwa, ya kuma
ce, ‘Kada ka ɗauko wa ɗana mata daga ’ya’ya matan Kan’aniyawa, waɗanda nake
zama a ƙasarsu, 38 amma ka tafi wajen gidan mahaifina da kuma dangina, ka ɗauko
wa ɗana mata.’

39 “Sai na ce wa maigidana, ‘A ce matar ba tă yarda tă zo tare da ni ba fa?’

40 “Maigidana ya ce, ‘Ubangiji wanda yake tare da ni zai aiki mala’ikansa tare da
kai, yă kuma sa tafiyarka tă yi nasara, don ka samo wa ɗana mata daga dangina,
daga kuma gidan mahaifina. 41 Ta haka za ka kuɓuta daga rantsuwata sa’ad da ka
tafi wurin dangina, ko ma sun ƙi su ba ka ita, za ka kuɓuta daga rantsuwata.’

42 “Sa’ad da na zo rijiya a yau, na ce, ‘Ya Ubangiji Allah na maigidana Ibrahim, ina
roƙonka ka ba ni nasara a tafiyar da na yi. 43 Duba, ina tsaye kusa da wannan rijiya;
in wata yarinya ta fito domin tă ɗiba ruwa, wadda in na ce mata, “Ina roƙonki bari
in ɗan sha ruwa daga tulunki,” 44 in ta ce, “Ka sha, zan kuma ba wa raƙumanka ma,”
bari tă zama wadda Ubangiji ya zaɓar wa ɗan maigidana.’
45 “Kafin in gama addu’ar, a zuciyata, sai ga Rebeka ta fito da tulunta a kafaɗarta.
Ta gangara zuwa rijiyar ta ɗebo ruwa, na kuma ce mata, ‘Ina roƙonki ki ba ni ɗan
ruwa daga tulunki.’
46 “Ta yi sauri ta saukar da tulun daga kafaɗarta ta ce, ‘Sha, zan kuma ba wa
raƙumanka su ma.’ Sai na sha, ta kuma shayar da raƙumana su ma.
47 “Na tambaye ta, ‘Ke ’yar wane ne?’
“Ta ce, ‘’Yar Betuwel ɗan Nahor, wanda Milka ta haifa masa.’
“Sai na sa mata zobe a hancinta, woroworo kuma a hannuwata, 48 na kuma sunkuya
na yi wa Ubangiji sujada. Na yabi Ubangiji Allah na maigidana Ibrahim wanda ya bi
da ni a hanyar da take daidai, don in samo wa ɗan maigidana jikanyar ɗan’uwansa.
49 Yanzu fa in za ku nuna wa maigidana alheri da aminci, ku faɗa mini, in kuma ba
haka ba, ku faɗa mini, don in san hanyar da zan juya.”
50 Laban da Betuwel suka ce, “Wannan daga wurin Ubangiji ne, ba abin da za mu
ce I, ko a’a ba. 51 Ga Rebeka, ɗauke ta ku tafi, bari tă zama matar ɗan maigidanka,
yadda Ubangiji ya umarta.”
52 Sa’ad da bawan Ibrahim ya ji abin da suka ce, sai ya rusuna har ƙasa a gaban
Ubangiji. 53 Sa’an nan bawan ya fito da kayan ado na zinariya da azurfa da kayayyaki
na tufafi ya ba wa Rebeka; ya kuma ba wa ɗan’uwanta da mahaifiyarta kyautai masu
tsada. 54 Sa’an nan shi da mutanen da suke tare da shi suka ci, suka sha, suka kuma
kwana a can.
Kashegari da safe da suka tashi sai ya ce, “A sallame ni in koma wurin maigidana.”
55 Amma ɗan’uwanta da mahaifiyarta suka ce, “Bari yarinyar ta ɗan zauna tare da
mu kwana goma ko fiye, sa’an nan ka* ta fi.”
56 Amma ya ce musu, “Kada ku tsai da ni, tun da Ubangiji ya ba ni nasara a tafiyata.
Ku sallame ni domin in tafi wurin maigidana.”
57 Sa’an nan suka ce, “Bari mu kira yarinyar mu tambaye ta game da zancen.”
58 Saboda haka suka kira Rebeka suka ce mata, “Za ki tafi tare da mutumin nan?”
Sai ta ce, “Zan tafi.”
59 Saboda haka suka sallame Rebeka, ’yar’uwarsu, duk da uwar goyonta da bawan
Ibrahim da mutanensa. 60 Suka kuma albarkaci Rebeka suka ce mata,
“’Yar’uwarmu, bari ki zama mahaifiyar
dubu dubbai,
bari zuriyarki su mallaki
ƙofofin abokan gābansu.”
61 Sa’an nan Rebeka da bayinta mata suka shirya suka hau raƙumansu suka koma
tare da mutumin. Da haka bawan ya ɗauki Rebeka ya tafi.
62 Ishaku kuwa ya zo daga Beyer-Lahai-Royi, gama yana zama a Negeb. 63 Wata
rana da yamma ya fita zuwa fili domin yă yi tunani†, sa’ad da ya ɗaga ido, sai ya
ga raƙuma suna zuwa. 64 Rebeka ma ta ɗaga ido sai ta ga Ishaku. Ta sauka daga
raƙuminta da sauri, 65 ta ce wa bawan, “Wane ne mutumin can a fili, da yake zuwa
yă tarye mu?”
Bawan ya ce, “Maigidana ne.” Saboda haka ta ɗauki mayafinta to rufe kanta.

* **24:55** Ko kuwa ta † **24:63** Ma’anar Ibraniyanci na wannan kalma ba a tabbatar ba.

66 Sai bawan ya faɗa wa Ishaku duk abin da ya yi. 67 Ishaku ya kawo ta cikin
tentin mahaifiyarsa Saratu, ya kuma auri Rebeka. Ta haka ta zama matarsa, ya kuwa
ƙaunace ta; Ishaku kuma ya ta'azantu bayan rasuwar mahaifiyarsa.

# 25

*Mutuwar Ibrahim*

1 Ibrahim ya auro wata mace, mai suna Ketura. 2 Ta haifa masa Zimran, Yokshan,
Medan, Midiyan, Ishbak da Shuwa. 3 Yokshan shi ne mahaifin Sheba da Dedan.
Zuriyar Dedan su ne mutanen Ashur, da mutanen Letush, da kuma mutanen
Lewummin. 4 'Ya'yan Midiyan maza su ne, Efa, Efer, Hanok, Abida, da kuma Elda'a.
Dukan waɗannan zuriyar Ketura ce.
5 Ibrahim ya bar wa Ishaku kome da ya mallaka. 6 Amma yayinda Ibrahim yake da
rai, ya ba wa 'ya'yan ƙwarƙwaransa maza kyautai, ya kuma sallame su daga ɗansa
Ishaku zuwa ƙasashen gabas.
7 Duka-duka, Ibrahim ya yi shekara ɗari da saba'in da biyar. 8 Sa'an nan Ibrahim
ya ja numfashinsa na ƙarshe, ya kuma mutu da kyakkyawar tsufa, tsoho da kuma
shekaru masu yawa; aka kuma tara shi ga mutanensa. 9 'Ya'yansa maza kuwa Ishaku
da Ishmayel suka binne shi cikin kogon Makfela, kusa da Mamre, a cikin filin Efron
ɗan Zohar mutumin Hitti, 10 filin da Ibrahim ya saya daga Hittiyawa. A nan aka binne
Ibrahim tare da matarsa Saratu. 11 Bayan rasuwar Ibrahim, Allah ya albarkaci ɗansa
Ishaku wanda a lokacin yana zama kusa da Beyer-Lahai-Royi.

*'Ya'yan Ishmayel maza*
*(1 Tarihi 1.28-31)*

12 Waɗannan su ne zuriyar Ishmayel ɗan Ibrahim, wanda Hagar mutuniyar Masar,
baranyar Saratu, ta haifa wa Ibrahim.

13 Ga jerin sunayen 'ya'yan Ishmayel maza bisa ga haihuwarsu,

Nebayiwot ɗan farin Ishmayel,
Kedar, Adbeyel, Mibsam,
14 Mishma, Duma, Massa,
15 Hadad, Tema, Yetur,
Nafish da Kedema.

16 Waɗannan su ne 'ya'yan Ishmayel maza, waɗanda kuma suke sunayen
kabilu goma sha biyu masu mulki bisa ga wuraren zamansu da sansaninsu.

17 Duka-duka Ishmayel ya yi shekara ɗari da talatin da bakwai; sai ya ja num-
fashinsa na ƙarshe, ya kuma mutu, aka kuma tara shi ga mutanensa. 18 Zuriyarsa
sun zauna tsakanin Hawila ne da Shur, wanda yake kusa da gabashin iyakar Masar
wajen Asshur. Sun yi zaman rikici da dukan sauran 'yan'uwansu.

*Haihuwar Yaƙub da Isuwa*

19 Waɗannan su ne zuriyar Ishaku ɗan Ibrahim.

Ibrahim ya haifi Ishaku, 20 Ishaku yana da shekara arba'in sa'ad da ya auri Rebeka
'yar Betuwel, mutumin Aram, daga Faddan Aram, 'yar'uwar Laban mutumin Aram.
21 Ishaku ya yi addu'a ga UBANGIJI a madadin matarsa, saboda ba ta haihuwa.
UBANGIJI ya amsa addu'arsa, matarsa Rebeka kuwa ta yi ciki. 22 Jariran suka kama
kokawa da juna a cikinta, sai ta ce, "Me ya sa wannan yake faruwa da ni?" Saboda
haka ta tafi don ta nemi nufin UBANGIJI.

23 UBANGIJI ya ce mata,
“Al’ummai biyu suna a cikin mahaifarki
mutum biyu da za ki haifa, za su rabu da juna,
ɗayan zai fi ɗayan ƙarfi,
babban kuma zai bauta wa ƙaramin.”
24 Da lokaci ya yi da za tă haihu, sai ga ’yan biyu maza a mahaifarta. 25 Wanda ya
fara fita ja ne, dukan jikinsa kuwa kamar riga mai gashi. Don haka aka sa masa suna
Isuwa. 26 Bayan wannan, ɗan’uwansa ya fito, da hannunsa yana riƙe da ɗiɗɗigen
Isuwa; don haka aka sa masa suna Yaƙub. Ishaku yana da shekara sittin, lokacin da
Rebeka ta haife su.
27 Yaran suka yi girma, Isuwa kuwa ya zama riƙaƙƙen maharbi, mutumin jeji,
yayinda Yaƙub, shiru-shiru ne mai son zama a tentuna. 28 Ishaku, mai son ci naman
jeji, ya ƙaunaci Isuwa, amma Rebeka ta ƙaunaci Yaƙub.
29 Wata rana sa’ad da Yaƙub yana dafa fate. Isuwa ya shigo daga jeji, da yunwa
sosai. 30 Ya ce wa Yaƙub, “Ina roƙonka, ka ɗan ɗiba mini faten nan! Ina fama da
yunwa!” (Shi ya sa aka kira shi Edom.)*
31 Yaƙub ya amsa ya ce, “Ka fara sayar mini da matsayinka na ɗan fari tukuna.”
32 Isuwa ya ce, “Duba, ina gab da mutuwa, me matsayina na ɗan fari zai yi mini?”
33 Amma Yaƙub ya ce, “Ka rantse mini tukuna.” Don haka ya rantse masa, ya sayar
da matsayinsa na ɗan fari ga Yaƙub.
34 Sa’an nan Yaƙub ya ba wa Isuwa burodi da ɗan miyan lansir. Ya ci, ya sha, sa’an
nan ya tashi ya tafi.
Ta haka Isuwa ya yi banza da matsayinsa na ɗan fari.

# 26

*Ishaku da Abimelek*
1 Aka yi yunwa a ƙasar; ban da yunwar da aka yi da fari a zamanin Ibrahim, sai
Ishaku ya tafi wurin Abimelek sarkin Filistiyawa a Gerar. 2 UBANGIJI kuwa ya bayyana
ga Ishaku ya ce, “Kada ka gangara zuwa Masar; ka yi zauna a ƙasar da zan faɗa maka.
3 Ka zauna a wannan ƙasa na ɗan lokaci, zan kuwa kasance tare da kai, zan kuma
albarkace ka. Gama zan ba da waɗannan ƙasashe gare ka da kuma zuriyarka. Zan
kuma cika rantsuwar da na yi wa mahaifinka Ibrahim. 4 Zan sa zuriyarka ta yi yawa
kamar taurari a sararin sama zan kuwa ba su dukan waɗannan ƙasashe, ta wurin
’ya’yanka kuma za a albarkaci dukan al’umman duniya, 5 domin Ibrahim ya yi mini
biyayya ya kuma kiyaye umarnaina, ƙa’idodina da kuma dokokina.” 6 Sai Ishaku ya
zauna a Gerar.
7 Sa’ad da mutanen wurin suka tambaye shi game da matarsa, sai ya ce, “’Yar’uwata
ce,” gama yana tsoro yă ce, “Ita matata ce.” Ya yi tunani, “Mutane wannan wuri za
su kashe ni ta dalili Rebeka, domin kyakkyawa ce.”
8 Sa’ad da Ishaku ya daɗe a can, sai Abimelek sarkin Filistiyawa ya duba daga taga
ya ga Ishaku yana rungumar matarsa Rebeka. 9 Saboda haka Abimelek ya aika Ishaku
yă je, sa’an nan ya ce, “Tabbatacce ita matarka ce! Me ya sa ka ce, ‘Ita ’yar’uwata
ce?’ ”
Ishaku ya amsa masa ya ce, “Don na yi tsammani zan rasa raina saboda ita.”
10 Sa’an nan Abimelek ya ce, “Me ke nan ka yi mana? Da a ce wani daga mazanmu
ya kwana da matarka, ai, da ka jawo laifi a kanmu.”
11 Saboda haka Abimelek ya yi umarni ga dukan mutane. “Duk wanda ya fitine
wannan mutum ko matarsa, tabbatacce za a kashe shi.”
12 Ishaku ya shuka hatsi a wannan ƙasa, a shekaran nan ya yi girbi ninki ɗari,
domin UBANGIJI ya albarkace shi. 13 Mutumin ya arzuta, arzikinsa ya yi ta haɓaka

* 25:30 Edom yana nufin ja.

har ya zama attajiri. 14 Ya kasance da garkunan tumaki da na shanu da bayi masu
yawa, har Filistiyawa suka yi ƙyashinsa. 15 Saboda haka dukan rijiyoyin da bayin
mahaifinsa suka haƙa a kwanakin da mahaifinsa Ibrahim yake da rai, Filistiyawa sun
toshe su, suka kuma ciccike su da ƙasa.
16 Sai Abimelek ya ce wa Ishaku, "Fita daga cikinmu; ka fi ƙarfinmu."
17 Saboda haka Ishaku ya fita daga can, ya yi sansani a Kwarin Gerar, ya kuma
zauna a can. 18 Ishaku ya sāke tona rijiyoyi waɗanda dā aka haƙa a zamanin Ibrahim
mahaifinsa, gama Filistiyawa suka tattoshe bayan mutuwar Ibrahim, ya kuma sa
musu sunayen da mahaifinsa ya ba su.
19 Barorin Ishaku suka haƙa cikin kwarin suka kuwa sami rijiya mai ruwa mai
kyau a can. 20 Amma makiyayan Gerar suka yi faɗa da na Ishaku suka ce, "Ruwan
namu ne!" Saboda haka Ishaku ya ba wa rijiyar suna Esek,* domin sun yi faɗa da
shi. 21 Sai suka haƙa wata rijiya, amma suka yi faɗa a kanta ita ma, saboda haka ya
ce da ita Sitna.† 22 Sai Ishaku ya matsa daga can ya sāke haƙa wata rijiyar, babu wani
kuma da yi faɗa a kanta. Sai ya ba ta suna Rehobot,‡ yana cewa, "Yanzu UBANGIJI ya
ba mu wuri, za mu kuwa yi ta haihuwa a ƙasar."
23 Daga can ya haura zuwa Beyersheba. 24 A wannan dare UBANGIJI ya bayyana
gare shi ya ce, "Ni ne Allah na mahaifinka Ibrahim. Kada ka ji tsoro, gama ina tare
da kai, zan albarkace ka, zan kuma ƙara yawan zuriyarka saboda bawana Ibrahim."
25 Sai Ishaku ya gina bagade a can, ya kuma kira bisa sunan UBANGIJI. A can ya
kafa tentinsa, a can kuma bayinsa suka haƙa wata rijiya.
26 Ana cikin haka, sai Abimelek ya zo wurinsa daga Gerar, tare da Ahuzzat mai ba
shi shawara da Fikol shugaban mayaƙansa. 27 Ishaku ya tambaye su, "Me ya kawo
ku gare ni, da yake kun yi gāba da ni, kuka kuma kore ni?"
28 Suka amsa, "Mun ga a zahiri cewa UBANGIJI yana tare da kai; saboda haka muka
ce, 'Dole rantsuwa ta kasance tsakaninmu da kai.' Bari mu yi yarjejjeniya da kai
29 cewa ba za ka cuce mu ba, kamar yadda ba mu fitine ka ba, amma muka yi
maka kirki, muka kuma sallame ka cikin salama. Yanzu kuwa kai albarkatacce ne
na UBANGIJI."
30 Sai Ishaku ya shirya musu liyafa, suka ci suka kuma sha. 31 Kashegari da sassafe
sai mutanen suka yi wa juna rantsuwa. Sa'an nan Ishaku ya sallame su, suka kuwa
tafi cikin salama.
32 A wannan rana bayin Ishaku suka zo suka faɗa masa game da rijiyar da suka
haƙa. Suka ce, "Mun sami ruwa!" 33 Sai ya kira ta Shiba,§ don haka har wa yau ana
kira garin Beyersheba.*
34 Sa'ad da Yaƙub ya kai shekaru arba'in da haihuwa, sai ya auri Yudit 'yar Beyeri
mutumin Hitti, da kuma Basemat 'yar Elon mutumin Hitti. 35 Su ne suka zama
sanadin baƙin ciki ga Ishaku da Rebeka.

# 27

*Yaƙub ya sami albarkar Ishaku*

1 Sa'ad da Ishaku ya tsufa idanunsa suka raunana har ba ya iya gani, sai ya kira
Isuwa babban ɗansa ya ce masa, "Ɗana."
Isuwa kuwa ya amsa, ya ce "Ga ni."
2 Ishaku ya ce, "Yanzu na tsufa kuma ban san ranar mutuwata ba. 3 Saboda haka
yanzu, ka ɗauki makamanka, kwari da bakanka, ka tafi jeji ka farauto mini nama.

* **26:20** Esek yana nufin rikici. † **26:21** Sitna yana nufin adawa. ‡ **26:22** Rehobot yana nufin ɗaki. § **26:33** Shiba yana iya nufin rantsuwa ko kuma bakwai. * **26:33** Beyersheba yana iya nufin rijiyar rantsuwa ko kuwa rijiyar bakwai.

4 Ka shirya mini irin abinci mai daɗin da nake so, ka kawo mini in ci, domin in sa maka albarka kafin in mutu."
5 Ashe, Rebeka tana ji sa'ad da Ishaku ya yi wa ɗansa Isuwa magana. Da Isuwa
ya tafi jeji don yă farauto nama yă kawo, 6 sai Rebeka ta ce wa ɗanta Yaƙub, "Ka
ji nan, na ji mahaifinka ya ce wa ɗan'uwanka Isuwa, 7 'Kawo mini nama ka shirya
mini abinci mai daɗi don in ci, in sa maka albarka a gaban UBANGIJI kafin in mutu.'
8 Saboda haka ɗana, ka saurara da kyau ka kuma yi abin da na faɗa maka. 9 Je garke
ka kawo mini awaki biyu kyawawa, domin in shirya abinci mai daɗi wa mahaifinka,
kamar yadda dai yake so. 10 Sa'an nan ka kai wa mahaifinka yă ci, domin yă sa maka
albarka kafin yă mutu."
11 Yaƙub ya ce wa mahaifiyarsa Rebeka, "Amma ɗan'uwana Isuwa mutum ne mai
gashi a jiki, ni kuma jikina sumul yake. 12 A ce baba ya tattaɓa ni fa? Zai zama kamar
ina ruɗunsa ne, wannan fa zai jawo mini la'ana a maimakon albarka."
13 Mahaifiyarsa ta ce masa, "Ɗana, bari la'anar tă fāɗo a kaina. Kai dai yi abin da
na faɗa, jeka ka kawo mini su."
14 Sai ya tafi ya kamo su, ya kawo wa mahaifiyarsa, ta kuwa shirya abinci mai daɗi,
yadda mahaifinsa yake so. 15 Sa'an nan Rebeka ta ɗauki riguna mafi kyau na Isuwa
babban ɗanta, waɗanda take da su a gida ta sa wa ƙaramin ɗanta Yaƙub. 16 Sai ta
mamanne gashin awakin nan biyu a hannuwansa da bayan wuyarsa wanda ba gashi.
17 Sa'an nan ta ba wa ɗanta Yaƙub abinci mai daɗi da kuma burodin da ta yi.
18 Shi kuwa ya tafi wurin mahaifinsa ya ce, "Babana."
Shi kuma ya amsa "I, ɗana, wane ne?"
19 Yaƙub ya ce wa mahaifinsa, "Ni ne Isuwa ɗan farinka. Na yi yadda ka faɗa mini.
Ina roƙonka tashi ka zauna ka ci naman, domin ka sa mini albarkarka."
20 Ishaku ya tambayi ɗansa, "Yaya aka yi ka samo shi da sauri haka, ɗana?"
Yaƙub ya amsa ya ce, "UBANGIJI Allahnka ne ya ba ni nasara."
21 Sai Ishaku ya ce wa Yaƙub, "Zo kusa don in taɓa ka, ɗana, domin in sani ko
tabbatacce kai ne ɗana Isuwa ko babu."
22 Yaƙub kuwa ya matsa kusa da mahaifinsa Ishaku, wanda ya tattaɓa shi, sa'an nan
ya ce, "Muryan nan dai, muryar Yaƙub ce, amma hannuwan, hannuwan Isuwa ne."
23 Bai gane shi ba, gama hannuwansa suna da gashi kamar na ɗan'uwansa Isuwa,
saboda haka ya albarkace shi. 24 Ya tambaya, "Tabbatacce kai ne ɗana Isuwa?"
Ya amsa ya ce "Ni ne."
25 Sa'an nan ya ce, "Ɗana, kawo mini naman da ka farauto in ci, domin in sa maka
albarka."
Yaƙub ya kawo masa ya kuwa ci; ya kuma kawo masa ruwan inabi ya kuma sha.
26 Sa'an nan mahaifinsa Ishaku ya ce masa, "Zo nan, ɗana ka sumbace ni."
27 Saboda haka ya je gunsa ya sumbace shi. Sa'ad da Ishaku ya ji ƙanshin rigunansa,
sai ya sa masa albarka ya ce,
"Aha, ƙanshin ɗana
yana kama da ƙanshin jejin
da UBANGIJI ya sa wa albarka ne.
28 Allah yă ba ka daga raɓar sama da kuma yalwar ƙasa,
yalwar hatsi da sabon ruwan inabi.
29 Bari al'ummai su bauta maka mutane kuma su rusuna maka.
Ka zama shugaba a kan 'yan'uwanka
bari kuma 'ya'yan mahaifiyarka su rusuna maka.
Bari waɗanda suka la'anta ka, su la'antu;
waɗanda kuma suka sa maka albarka, su sami albarka."
30 Bayan Ishaku ya gama sa masa albarka, Yaƙub yana fita daga mahaifinsa ke nan,
sai ga ɗan'uwansa Isuwa ya dawo daga farauta. 31 Shi ma ya shirya abinci mai daɗi

ya kawo wa mahaifinsa. Sa'an nan ya ce masa, "Babana, tashi ka zauna ka ci daga abin da na farauto, domin ka sa mini albarka."
32 Mahaifinsa Ishaku ya tambaye shi, "Wane ne kai?"
Ya amsa, "Ni ne ɗanka, ɗan farinka, Isuwa."
33 Ishaku ya yi makyarkyata ƙwarai ya ce, "To, wane ne wannan da ya farauto nama ya kawo mini kafin ka zo, har na ci na kuma sa masa albarka? Tabbatacce zai zama mai albarka!"
34 Sa'ad da Isuwa ya ji kalmomin mahaifinsa, sai ya fashe da kuka mai zafi kuma da ƙarfi, ya ce wa mahaifinsa, "Ka albarkace ni, ni ma, baba!"
35 Amma ya ce, "Ɗan'uwanka ya zo da makirci ya karɓi albarkarka."
36 Isuwa ya ce, "Ba saboda haka ne aka raɗa masa suna Yaƙub* ba? Ya yi mini ƙwace sau biyu ke nan; ya ƙwace mini matsayina na ɗan fari, ga shi yanzu kuma ya karɓi albarkata." Sa'an nan ya yi tambaya, "Ba sauran albarkar da ka rage mini?"
37 Ishaku ya amsa wa Isuwa, "Na mai da shi shugaba a kanka, na sa dukan dangoginsa su zama bayinsa, na kuma ba shi hatsi da sabon ruwan inabi. Saboda haka me kuma zan yi maka ɗana?"
38 Isuwa ya ce wa mahaifinsa, "Iyakar albarkar da kake da ita ke nan, baba? Ka albarkace ni ni ma, baba!" Sai Isuwa ya ɗaga murya ya yi kuka.
39 Mahaifinsa Ishaku ya amsa masa ya ce,
"Ga shi, ni'imar ƙasar za tă
nisanci mazauninka.
Raɓar samaniya can ƙwanƙoli za
tă nisance ka.
40 Za ka rayu ta wurin takobi
za ka kuwa bauta wa ɗan'uwanka.
Amma sa'ad da ka ɓalle,
za ka kakkarye karkiyarsa
daga wuyanka."

*Yaƙub ya gudu zuwa wurin Laban*

41 Isuwa ya riƙe Yaƙub a zuciya saboda albarkar da mahaifinsa ya sa masa. Ya ce wa kansa, "Kwanakin mutuwar mahaifina sun yi kusa; sa'an nan zan kashe ɗan'uwana Yaƙub."
42 Sa'ad da aka faɗa wa Rebeka abin da babban ɗanta Isuwa ya faɗa, sai ta kira ɗanta Yaƙub ta ce masa, "Ɗan'uwanka Isuwa yana ta'azantar da kansa da tunanin kashe ka. 43 To, fa, ɗana, yi abin da na ce; gudu nan take zuwa wurin ɗan'uwana
Laban a Haran. 44 Zauna tare da shi na ɗan lokaci sai ɗan'uwanka ya huce. 45 Sa'ad
da ɗan'uwanka ya daina fushi da kai, ya kuma manta da abin da ka yi masa, zan aika don ka dawo daga can. Don me zan rasa ku biyu a rana guda?"
46 Sa'an nan Rebeka ta ce wa Ishaku, "Ni fa na gaji da matan Hittiyawan nan. In Yaƙub ya auri mata daga cikin matan ƙasan nan, wato, daga matan Hittiyawa irin waɗannan, rayuwata ba za tă daɗa mini kome ba."

# 28

1 Saboda haka Ishaku ya kira Yaƙub, ya kuma albarkace* shi, sa'an nan ya umarce shi ya ce, "Kada ka auri mace daga Kan'ana. 2 Tashi nan da nan ka tafi Faddan
Aram,† zuwa gidan mahaifin mahaifiyarka Betuwel. Ka ɗauko wa kanka mata a can daga cikin 'ya'ya matan Laban ɗan'uwan mahaifiyarka. 3 Bari Allah Maɗaukaki‡ yă
albarkace ka, yă kuma sa ka yi ta haihuwa ka riɓaɓɓanya har ka zama ƙungiyar

* 27:36 Yaƙub yana nufin ya kama ɗiɗɗigi, a habaici ya yi ruɗu. * 28:1 Ko kuwa gaishe † 28:2 Wato, arewa maso gabashin Mesofotamiya, haka ma a ayoyi 5, 6 da 7 ‡ 28:3 Da Ibraniyanci El-Shaddai.

jama'o'i. 4 Bari Allah yǎ ba ka da kuma zuriyarka albarkar da ya ba wa Ibrahim,
don ka amshi ƙasar da kake baƙunci, ƙasar da Allah ya ba wa Ibrahim." 5 Sa'an
nan Ishaku ya sallami Yaƙub, ya kuwa tafi Faddan Aram, zuwa wurin Laban ɗan
Betuwel mutumin Aram. Laban ne ɗan'uwan Rebeka, wadda take mahaifiyar Yaƙub
da Isuwa.
6 Yanzu Isuwa ya san cewa Ishaku ya albarkaci Yaƙub ya kuma aike shi zuwa
Faddan Aram don yǎ auri mata daga can, ya kuma san cewa sa'ad da ya albarkace
shi, ya umarce shi cewa, "Kada ka auro wata mace daga cikin Kan'aniyawa," 7 ya
kuma san cewa Yaƙub ya yi biyayya da mahaifinsa da kuma mahaifiyarsa, ya kuwa
tafi Faddan Aram. 8 Sai Isuwa ya gane cewa matan Kan'aniyawa ba su gamshi
mahaifinsa Ishaku ba; 9 saboda haka sai ya tafi wurin Ishmayel ya auri Mahalat,
'yar'uwar Nebayiwot da kuma 'yar Ishmayel ɗan Ibrahim, ban da matan da yake da
su.

### *Mafarkin Yaƙub a Betel*

10 Yaƙub ya bar Beyersheba ya kama hanyar Haran. 11 Sa'ad da ya kai wani wuri,
sai ya dakata domin yǎ kwana, gama rana ta riga ta fāɗi. Ya ɗauki dutse daga
cikin duwatsun wurin, ya sa shi ya zama matashin kansa, sa'an nan ya kwanta
don yǎ yi barci. 12 Ya yi mafarki inda ya ga wata matakalar hawa,§ tsaye a ƙasa,
kanta ta kai sama, mala'ikun Allah kuwa suna hawa, suna sauka a kanta. 13 A can
bisanta*UBANGIJI ya tsaya, ya kuma ce, "Ni ne UBANGIJI Allah na mahaifinka Ibrahim
da kuma Allah na Ishaku. Zan ba ka, kai da kuma zuriyarka, ƙasar da kake kwance
a kai. 14 Zuriyarka za tǎ zama kamar ƙurar ƙasa, za ka kuma bazu zuwa yamma da
kuma gabas, zuwa arewa da kuma kudu. Dukan mutanen duniya za su sami albarka
ta wurinka da kuma ta wurin 'ya'yanka. 15 Ina tare da kai, zan lura da kai duk inda
ka tafi, zan kuma dawo da kai zuwa wannan ƙasa. Ba zan rabu da kai ba sai na cika
abin da na yi maka alkawari."
16 Sa'ad da Yaƙub ya farka daga barci, sai ya yi tunani ya ce, "Tabbatacce UBANGIJI
yana a wannan wuri, ban kuwa sani ba." 17 Ya ji tsoro, ya kuma ce, "Wane irin wuri
ne mai banrazana haka! Lalle wannan gidan Allah ne, kuma nan ne ƙofar sama."
18 Kashegari da sassafe, sai Yaƙub ya ɗauki dutsen da ya yi matashin kai da shi, ya
kafa shi al'amudi, ya kuma zuba mai a kansa. 19 Ya kira wannan wuri Betel† ko da
yake dā ana kiran birnin Luz ne.
20 Sa'an nan Yaƙub ya yi alkawari cewa, "In Allah zai kasance tare da ni yǎ kuma
lura da ni a wannan tafiya, yǎ kuma ba ni abinci in ci da tufafi in sa, 21 har in dawo
lafiya zuwa gidan mahaifina, to, UBANGIJI‡ zai zama Allahna 22 kuma§ wannan dutsen
da na kafa al'amudi, zai zama gidan Allah, kuma dukan abin da ka ba ni zan ba ka
kashi ɗaya bisa goma."

# 29

### *Yaƙub ya isa Faddan Aram*

1 Sa'an nan Yaƙub ya ci gaba da tafiyarsa har ya kai ƙasar mutanen gabashi. 2 A can
ya ga rijiya a jeji da garkuna uku na tumaki kwance kusa da ita, gama a wannan rijiya
ce ake shayar da garkuna. Dutsen da ake rufe bakin rijiyar mai girma ne. 3 Sa'ad
da dukan garkuna suka taru a can, sai makiyayan su gungurar da dutsen daga bakin
rijiyar su shayar da tumaki. Sa'an nan su mai da dutsen a wurinsa a bakin rijiya.
4 Yaƙub ya tambayi makiyayan ya ce, "'Yan'uwa, ina kuka fito?"
Suka amsa, "Mu daga Haran ne."

---

§ **28:12** Ko tsani. * **28:13** Ko kuwa can kusa da shi † **28:19** Betel yana nufin gidan Allah. ‡ **28:21** Ko kuwa Da yake Allah… gidan mahaifina, UBANGIJI § **28:22** Ko kuwa gida, UBANGIJI, kuwa zai zama Allahna, sa'an nan. 22 Kuma

5 Sai ya ce musu, “Kun san Laban, jikan Nahor?”
Suka amsa, “I, mun san shi.”
6 Sa’an nan Yaƙub ya tambaye su, “Yana nan lafiya?”
Suka ce, “I, yana lafiya, ga ma ’yarsa Rahila tafe da tumaki.”
7 Ya ce, “Duba har yanzu da sauran rana da yawa, lokaci bai kai na tara garkuna
ba. Ku shayar da tumaki ku mai da su wurin kiwo.”
8 Suka amsa suka ce, “Ba za mu iya ba, sai dukan garkunan sun taru, aka kuma
gungurar da dutsen daga bakin rijiyar. Sa’an nan za mu shayar da tumakin.”
9 Tun yana cikin magana da su, sai ga Rahila ta zo da tumakin mahaifinta, gama ita
makiyayyiya ce. 10 Sa’ad da Yaƙub ya ga Rahila ’yar Laban, ɗan’uwan mahaifiyarsa,
da tumakin Laban, sai ya tafi ya gungurar da dutsen daga bakin rijiyar, ya kuma
shayar da tumakin kawunsa. 11 Sa’an nan Yaƙub ya sumbaci Rahila, ya kuma ɗaga
murya ya yi kuka. 12 Ya riga ya faɗa wa Rahila cewa shi dangin mahaifinta ne kuma
ɗan Rebeka. Saboda haka ta ruga da gudu ta faɗa wa mahaifinta.
13 Nan da nan, da Laban ya sami labari game da Yaƙub, ɗan ’yar’uwarsa, ya
gaggauta yă sadu da shi. Sai ya rungume shi ya sumbace shi, ya kuma kawo shi
gidansa, a can kuwa Yaƙub ya faɗa masa dukan waɗannan abubuwa. 14 Sa’an nan
Laban ya ce masa, “Kai nama da jinina ne.”

## *Yaƙub ya auri Liyatu da Rahila*

Bayan Yaƙub ya zauna da shi na wata guda cif, 15 sai Laban ya ce masa, “Don
kawai kai dangina ne na kusa, sai kawai ka yi mini aiki a banza? Faɗa mini abin da
albashinka zai zama.”
16 Laban dai yana da ’ya’ya mata biyu; sunan babbar Liyatu, sunan ƙaramar kuwa
Rahila. 17 Liyatu tana da raunannun* idanu, amma Rahila dai tsarinta yana da kyau
kuma kyakkyawa ce. 18 Yaƙub ya ƙaunaci Rahila, sai ya ce, “Zan yi maka aiki na
shekaru bakwai domin ƙaramar ’yarka Rahila.”
19 Laban ya ce, “Ya fi kyau in ba ka ita, da in ba wani mutum dabam. Zauna tare da
ni.” 20 Saboda haka Yaƙub ya yi bauta shekaru bakwai domin a ba shi Rahila, amma
shekarun suka zama kamar ’yan kwanaki ne kawai gare shi saboda ƙaunar da yake
mata.
21 Sa’an nan Yaƙub ya ce wa Laban, “Ba ni matata. Lokacina ya cika, ina kuma so
in kwana da ita.”
22 Saboda haka Laban ya tara dukan mutanen wurin, ya yi biki. 23 Amma da yamma
ta yi, sai ya ɗauki ’yarsa Liyatu ya ba da ita ga Yaƙub, sai Yaƙub ya kwana da ita.
24 Laban kuma ya ba da baranyarsa Zilfa wa ’yarsa tă zama mai hidimarta.
25 Sa’ad da safiya ta yi, sai ga Liyatu! Saboda haka Yaƙub ya ce wa Laban, “Mene
ne ke nan ka yi mini? Na yi maka bauta domin Rahila, ba haka na yi ba? Don me ka
ruɗe ni?”
26 Laban ya amsa, “Ba al’adarmu ba ce a nan a ba da ’ya ƙarama aure kafin ’yar
fari. 27 Ka gama makon amaryanci na ’yar nan; sa’an nan za mu ba ka ƙaramar ita
ma, don ƙarin waɗansu shekaru bakwai na aiki.”
28 Haka kuwa Yaƙub ya yi. Ya gama mako guda da Liyatu, sa’an nan Laban ya ba
shi ’yarsa Rahila tă zama matarsa. 29 Laban ya ba da baranyarsa Bilha wa ’yarsa
Rahila ta zama mai hidimarta. 30 Yaƙub ya kwana da Rahila ita ma, ya kuwa ƙaunaci
Rahila fiye da Liyatu. Ya kuma yi wa Laban aiki na ƙarin waɗansu shekaru bakwai.

## *’Ya’yan Yaƙub*

* **29:17** Ko kuwa mai laulayi

31 Sa'ad da UBANGIJI ya ga ba a ƙaunar Liyatu, sai ya buɗe mahaifarta, amma Rahila
ta zama bakararriya. 32 Sai Liyatu ta yi ciki ta haifi ɗa. Ta sa masa suna Ruben,† gama
ta ce, "Domin UBANGIJI ya ga wahalata. Tabbatacce mijina zai ƙaunace ni yanzu."
33 Ta sāke yin ciki, sa'ad da kuma ta haifi ɗa sai ta ce, "Gama UBANGIJI ya ji cewa
ba a ƙaunata, ya ba ni wannan shi ma." Saboda haka ta ba shi suna Simeyon.‡
34 Har yanzu ta yi ciki, sa'ad da kuma ta haifi ɗa sai ta ce, "Yanzu, a ƙarshe mijina
zai manne mini, gama na haifa masa 'ya'ya maza uku." Saboda haka ta ba shi suna
Lawi.§
35 Ta sāke yin ciki, sa'ad da ta haifi ɗa sai ta ce, "A wannan lokaci zan yabi
UBANGIJI." Saboda haka ta ba shi suna Yahuda.* Sa'an nan ta daina haihuwa.

# 30

1 Sa'ad da Rahila ta ga cewa ba tă haifa wa Yaƙub 'ya'ya ba, sai ta fara kishin
'yar'uwarta. Saboda haka ta ce wa Yaƙub, "Ka ba ni 'ya'ya, ko kuwa in mutu!"
2 Yaƙub ya fusata da ita ya ce, "Ina a matsayin Allah ne wanda ya hana ke samun
'ya'ya?"
3 Sa'an nan ta ce, "Ga Bilha, mai baiwata, ka kwana da ita don tă haifa mini 'ya'ya,
ta gare ta kuwa ni ma in gina iyali."
4 Saboda haka ta ba shi baranyarta Bilha tă zama matarsa. Yaƙub kuwa ya kwana
da ita, 5 ta kuwa yi ciki, ta kuma haifi ɗa. 6 Sa'an nan Rahila ta ce, "Allah ya baratar
da ni; ya saurari roƙona ya kuma ba ni ɗa." Saboda wannan ta ba shi suna Dan.*
7 Baranyar Rahila ta sāke yin ciki ta kuma haifi wa Yaƙub ɗa na biyu. 8 Sai Rahila
ta ce, "Na yi kokawa sosai da 'yar'uwata, na kuwa yi nasara." Saboda haka ta kira
shi Naftali.†
9 Sa'ad da Liyatu ta ga cewa ta daina haihuwa, sai ta ɗauki mai hidimarta Zilfa ta
ba da ita ga Yaƙub tă zama matarsa. 10 Baranyar Liyatu, Zilfa ta haifa wa Yaƙub ɗa.
11 Sai Liyatu ta ce, "Na yi sa'a!" Saboda haka ta ba shi suna Gad.‡
12 Zilfa baranyar Liyatu ta haifa wa Yaƙub ɗa na biyu. 13 Sai Liyatu ta ce, "Ni mai
farin ciki ce! Mata za su ce da ni mai farin ciki." Saboda haka ta sa masa suna Asher.§
14 A lokacin girbin alkama, sai Ruben ya je jeji ya ɗebo manta-uwa ya kawo wa
mahaifiyarsa Liyatu. Sai Rahila ta ce wa Liyatu, "Ina roƙonki ki ɗan sam mini manta-uwa ɗanki."
15 Amma ta ce mata, "Bai ishe ki ba ne da kika ƙwace mijina? Yanzu kuma kina so
ki ƙwace manta-uwa na yarona?"
Sai Rahila ta ce "Shi ke nan, mijina zai iya kwana da ke yau saboda manta-uwa na ɗanki."
16 Saboda haka sa'ad da Yaƙub ya dawo daga jeji a wannan yamma sai Liyatu ta
fito ta tarye shi. Ta ce, "Dole ka kwana da ni, na yi hayarka da manta-uwa na ɗana."
Saboda haka ya kwana da ita a wannan dare.
17 Allah ya saurari Liyatu, ta kuwa yi ciki ta kuma haifa wa Yaƙub ɗa na biyar.
18 Sai Liyatu ta ce, "Allah ya sāka mini saboda na ba da mai hidimata ga mijina."
Saboda haka ta ba shi suna Issakar.*
19 Liyatu ta sāke yin ciki ta kuma haifa wa Yaƙub ɗa na shida. 20 Sai Liyatu ta ce,
"Allah ya ba ni kyauta mai daraja. A wannan lokaci mijina zai darajarta ni, domin
na haifa masa 'ya'ya maza shida." Saboda haka ta ba shi suna Zebulun.†

† **29:32** Ruben ya yi kamar Ibraniyanci na, ya ga wahalata; sunan yana nufin duba, ɗa. ‡ **29:33** Simeyon mai yiwuwa yana nufin wanda yake ji. § **29:34** Lawi ya yi kamar, kuma za a iya ɗauka daga Ibraniyanci a matsayin manne. * **29:35** Yahuda ya yi kamar, kuma za a iya ɗauka daga Ibraniyanci a matsayin Yabo. * **30:6** Dan a nan yana nufin an baratar. † **30:8** Naftali yana nufin famata. ‡ **30:11** Gad zai iya nufin, sa'a ko kuwa ƙungiya. § **30:13** Asher yana nufin farin ciki. * **30:18** Issakar ya yi kamar Ibraniyanci na lada. † **30:20** Zebulun mai yiwuwa yana nufin daraja.

21 Daga baya ta haifi ʼya ta kuwa ba ta suna Dina.
22 Sai Allah ya tuna da Rahila; ya saurare ta ya kuma buɗe mahaifarta. 23 Sai ta yi
ciki ta kuma haifi ɗa ta ce, "Allah ya ɗauke mini kunyata." 24 Ta ba shi suna Yusuf,‡
ta kuma ce, "Bari UBANGIJI yă ƙara mini wani ɗa."

### *Garkunan Yaƙub sun ƙaru*

25 Bayan Rahila ta haifi Yusuf, sai Yaƙub ya ce wa Laban, "Ka sallame ni don in
koma ƙasata. 26 Ba ni matana da ʼyaʼyana, waɗanda na bauta maka dominsu, zan
kuwa tafi. Ka dai san yadda na bauta maka."
27 Amma Laban ya ce masa, "In na sami tagomashi daga gare ka, ina roƙonka ka
zauna. Na gane ta wurin duba cewa§UBANGIJI ya albarkace ni saboda kai." 28 Ya ƙara
da cewa, "Faɗa albashinka, zan kuwa biya shi."
29 Yaƙub ya ce masa, "Ka dai san yadda na yi maka aiki da kuma yadda dabbobinka
suka yi yawa a hannuna. 30 Kaɗan da kake da shi kafin zuwata ya ƙaru sosai, kuma
UBANGIJI ya albarkace ka a duk inda na tafi. Amma yanzu, yaushe zan yi wani abu
domin gidana ni ma?"
31 Sai Laban ya yi tambaya, "Me zan ba ka?"
Yaƙub ya amsa ya ce, "Kada ka ba ni wani abu. Amma in za ka yi mini abu guda
ɗaya, zan ci gaba da kiwon garkunanka, ina kuma lura da su. 32 Bari in ratsa cikin
dukan garkunanka yau in fid da masu dabbare-dabbare da tumaki babare-babare,
da kowane ɗan rago baƙi, da dabbare-dabbare da babare-babare na awaki daga ciki,
waɗannan ne za su zama ladana. 33 Gaskiyata kuwa za tă zama mini shaida nan
gaba, duk saʼad da ka bincika a kan albashin da ka biya ni. Duk akuyar da take tawa
da ba dabbare-dabbare ko babare-babare, ko ɗan ragon da ba baƙi ba, zai kasance
sata na yi."
34 Sai Laban ya ce, "Na yarda. Bari yă zama yadda ka faɗa." 35 A wannan rana ya
ware dukan bunsurai da suke dabbare-dabbare da masu zāne-zāne, da dukan awakin
da suke dabbare-dabbare (duka da suke da fari-fari a jikinsu), da dukan baƙaƙen
tumaki, ya sa su a hannun ʼyaʼyansa maza. 36 Saʼan nan ya sa nisan tafiya kwana
uku tsakaninsa da Yaƙub, yayinda Yaƙub ya ci gaba da lura da sauran garkunan
Laban Yaƙub.
37 Yaƙub ya samo ɗanyen reshen itatuwan aduruku, da na katambiri, da na durumi,
ya ɓare ya bar fararen cikin katakon rassan. 38 Saʼan nan ya zuba ɓararre rassan
cikin dukan kwamame na banruwa saboda su kasance a gaban garkunan saʼad da
suka zo shan ruwa. A saʼad da garkunan suke barbara suka kuma zo shan ruwa,
39 sai su yi barbara a gaban rassan. Sai kuwa su haifi ƙanana masu zāne dabbare-
dabbare, ko babare-babare ko masu zāne-zāne. 40 Sai Yaƙub yă ware ƙananan garken
dabam, amma sai yă sa sauran su fuskanci dabbobin da suke dabbare-dabbare da
kuma baƙaƙe da suke na Laban. Ta haka ya ware garkuna dabam domin kansa
bai kuwa haɗa su da dabbobin Laban ba. 41 A duk saʼad da ƙarfafa dabbobi mata
suke barbara, Yaƙub yakan zuba rassan a kwamame a gaban dabbobin saboda su yi
barbara kusa da rassan, 42 amma in dabbobin raunana ne, ba ya sa su a can. Saboda
haka raunanan dabbobi suka zama na Laban, ƙarfafan kuma suka zama na Yaƙub.
43 Ta haka mutumin ya zama riƙaƙƙe mai arziki, ya kasance mai manya-manyan
garkuna, da bayi mata da maza, da raƙuma da kuma jakuna.

# 31

### *Yaƙub ya gudu daga wurin Laban*

‡ **30:24** Yusuf mai yiwuwa yana nufin ya ƙara. § **30:27** Ko kuwa mai yiwuwa ya arzuta da kuma

1 Yaƙub ya ji cewa ʼyaʼya Laban mazan suna cewa, “Yaƙub ya kwashe dukan abin
da mahaifinmu yake da shi, ya kuma sami dukan wannan arziki daga abin da yake
na mahaifinmu.” 2 Yaƙub kuma ya lura cewa halin Laban gare shi ya canja ba kamar
yadda yake a dā ba.
3 Sai UBANGIJI ya ce wa Yaƙub, “Koma ƙasar kakanninka da kuma danginka, zan
kuwa kasance tare da kai.”
4 Saboda haka Yaƙub ya aika a ce wa Rahila da Liyatu su zo jeji inda garkunan suke.
5 Sai ya ce musu, “Na ga cewa halin mahaifinku gare ni ba kamar yadda dā yake ba,
amma Allah na mahaifina yana tare da ni. 6 Kun san cewa na yi aiki wa mahaifinku
da dukan ƙarfina, 7 duk da haka mahaifinku ya cuce ni ta wurin sauya albashina sau
goma. Amma dai, Allah bai yardar masa yă yi mini lahani ba. 8 In ya ce, ‘Dabbare-
dabbare ne za su zama ladanka,’ sai dukan garkunan su haifi dabbare-dabbare, in
kuma ya ce, ‘Masu zāne-zāne ne za su zama ladanka,’ sai dukan garkunan su haifi
ƙananan masu zāne-zāne. 9 Ta haka Allah ya kwashe dabbobin mahaifinku ya ba ni.
10 “A lokacin ɗaukar cikin garken, na taɓa yin mafarki inda na ga bunsuran da
suke barbara da garken, masu dabbare-dabbare, ko babare-babare, ko masu zāne-
zāne ne. 11 Sai malaʼikan Allah ya ce mini a mafarkin, ‘Yaƙub.’ Sai na amsa na ce,
‘Ga ni.’ 12 Ya ce, ‘Daga idanunka ka gani, dukan bunsuran da suke hawan garken,
masu dabbare-dabbare, ko babare-babare, ko masu zāne-zāne ne, gama na ga dukan
abin da Laban yake yin maka. 13 Ni ne Allah na Betel, inda ka zuba wa alʼamudi mai,
da kuma inda ka yi mini alkawari. Yanzu ka bar wannan ƙasa nan take, ka koma
ƙasarka ta ainihi.’ ”
14 Sai Rahila da Liyatu suka amsa suka ce, “Muna da wani rabo a gādon kayan
mahaifinmu ne? 15 Ba kamar baƙi ne yake ɗaukarmu ba? Ba sayar da mu kaɗai
ya yi ba, har ma ya yi amfani da abin da aka biya saboda mu. 16 Tabbatacce dukan
dukiyar da Allah ya kwashe daga mahaifinmu ya zama namu da ʼyaʼyanmu. Saboda
haka ka yi duk abin da Allah ya faɗa maka.”
17 Saʼan nan Yaƙub ya sa ʼyaʼyansa da matansa a kan raƙuma, 18 ya kuma kora
dukan dabbobinsa, suka ja gabansa, tare da dukan abubuwan da ya samu a Faddan
Aram,* don su tafi wurin mahaifinsa Ishaku a ƙasar Kanʼana.
19 Saʼad da Laban ya tafi don askin tumakinsa, sai Rahila ta sace gumakan gidan
mahaifinta. 20 Yaƙub kuwa ya ruɗe Laban mutumin Aram da bai sanar da shi zai
gudu ba. 21 Saboda haka ya gudu da dukan abin da ya mallaka, ya ƙetare Kogi,† ya
nufi yankin tuddan Gileyad.

### *Laban ya bi bayan Yaƙub*

22 A rana ta uku, sai aka faɗa wa Laban cewa Yaƙub ya gudu. 23 Sai Laban ya
ɗauki danginsa tare da shi, ya bi bayan Yaƙub har kwana bakwai, ya kuma same shi
a yankin tuddan Gileyad. 24 Sai Allah ya bayyana ga Laban mutumin Aram a mafarki
da dare, ya ce masa, “Ka yi hankali kada ka faɗa wa Yaƙub wani abu, ko mai kyau
ko marar kyau.”
25 Yaƙub ya riga ya kafa tentinsa a yankin tuddan Gileyad saʼad da Laban ya same
shi. Laban da danginsa suka kafa sansani a can su ma. 26 Sai Laban ya ce wa Yaƙub,
“Me ke nan ka yi? Ka ruɗe ni, ka kuma ɗauki ʼyaʼyana mata kamar kamammun
yaƙi. 27 Me ya sa ka gudu a ɓoye ka kuma ruɗe ni? Me ya sa ba ka faɗa mini don
in sallame ka da farin ciki da waƙoƙi haɗe da kiɗin ganguna da garayu ba? 28 Ba ka
ma bari in sumbaci jikokina da ʼyaʼyana mata in yi musu bankwana ba. Ka yi wauta.
29 Ina da iko in cuce ka; amma jiya da dare Allahn mahaifinka ya faɗa mini, ‘Ka yi
hankali kada ka faɗa wa Yaƙub wani abu ko mai kyau ko marar kyau.’ 30 Yanzu ka

* **31:18** Wato, arewa maso gabashin Mesofotamiya † **31:21** Wato, Yuferites

gudu domin kana marmari komawa gidan mahaifinka. Amma don me ka sace mini gumakana?"
31 Yaƙub ya amsa wa Laban, "Na ji tsoro ne, domin na yi tsammani za ka ƙwace
'ya'yanka mata daga gare ni ƙarfi da yaji. 32 Amma in ka sami wani wanda yake da
gumakanka, ba zai rayu ba. Kai da kanka ka duba a gaban danginmu, ko akwai wani abin da yake naka a nan tare da ni; in ka gani, ka ɗauka." Yaƙub dai bai san cewa Rahila ta sace gumakan ba.
33 Saboda haka Laban ya shiga tentin Yaƙub, ya shiga tentin Liyatu da kuma tentuna matan nan biyu bayi, amma bai sami kome ba. Bayan ya fita daga tentin Liyatu, sai
ya shiga tentin Rahila. 34 Rahila fa ta kwashe gumakan gidan ta sa su cikin sirdin raƙumi, ta kuma zauna a kansu. Laban ya bincika cikin kowane abu a tentin amma bai sami kome ba.
35 Sai Rahila ta ce wa mahaifinta, "Kada ka yi fushi, ranka yă daɗe da ban tashi tsaye a gabanka ba; gama ina al'adar mata ne." Saboda haka ya bincika amma bai sami gumakan gidan ba.
36 Yaƙub ya fusata, ya kuma yi wa Laban faɗa. Ya tambayi Laban, "Mene ne laifina?
Wanda zunubi na yi da kake farautata? 37 Yanzu da ka bincika dukan kayayyakina,
me ka samu da yake na gidanka? Kawo shi nan a gaban danginka da kuma dangina, bari su zama alƙali tsakaninmu biyu.
38 "Na kasance tare da kai shekaru ashirin. Tumakinka da awakinka ba su yi ɓarin
ciki ba, ban kuwa ci raguna daga garkunanka ba. 39 Ban kawo dabbobinka da namun
jeji suka yayyaga; na kuma ɗauki hasarar ba? Ka nemi in biya dukan abin da aka
sace da rana ko da dare. 40 Yanayin da na kasance ke nan, da rana na sha zafin rana
da dare kuma na sha sanyi, ga rashin barci. 41 Haka ya kasance shekaru ashirin da na
yi a gidanka. Na yi maka aiki shekaru goma sha huɗu domin 'ya'yanka mata biyu, na
kuma yi shekaru shida domin garkunanka, ka kuma canja albashina sau goma. 42 Da
ba don Allah na mahaifina, Allah na Ibrahim da kuma Tsoron Ishaku ya kasance tare da ni ba, tabbatacce da ka sallame ni hannu wofi. Amma Allah ya ga wahalata da famar hannuwana, ya kuwa tsawata maka da dare jiya."
43 Laban ya amsa wa Yaƙub, "Matan, 'ya'yana ne, 'ya'yansu, 'ya'yana ne, garkunan kuma garkunana ne. Dukan abin da kake gani, nawa ne. Duk da haka me zan yi a
rana ta yau ga waɗannan 'ya'yana mata, ko kuma ga 'ya'yan da suka haifa? 44 Zo,
bari mu ƙulla yarjejjeniya, da kai da ni, bari kuma ta kasance shaida a tsakaninmu."
45 Saboda haka Yaƙub ya ɗauki dutse ya kafa yă zama al'amudi. 46 Ya ce wa
danginsa. "Ku tattara waɗansu duwatsu." Sai suka kwashe duwatsu suka tsiba,
suka kuwa ci abinci a can kusa da tsibin. 47 Laban ya sa masa suna Yegar Sahaduta,‡
Yaƙub kuwa ya kira shi Galeyed.§
48 Laban ya ce, "Wannan tsibi, shi ne shaida tsakaninka da ni a yau." Shi ya sa
aka kira shi Galeyed. 49 Aka kuma kira shi Mizfa,* domin ya ce, "UBANGIJI yă sa ido
tsakanin ni da kai sa'ad da muka rabu da juna. 50 Laban ya ce in ka wulaƙanta 'ya'yana mata, ko ka auri waɗansu mata ban da 'ya'yana mata, ko da yake babu wani da yake tare da mu, ka tuna cewa Allah shi ne shaida tsakaninka da ni."
51 Laban ya kuma ce wa Yaƙub, "Ga wannan tsibi, ga kuma wannan al'amudin
da na kafa tsakaninka da ni. 52 Wannan tsibin shi ne shaida, wannan al'amudi kuma shaida ne, cewa ba zan tsallake wannan tsibi zuwa gefenka don in cuce ka ba, kai kuma ba za ka tsallake wannan tsibi da al'amudi zuwa gefena don ka cuce
ni ba. 53 Bari Allah na Ibrahim da Allah na Nahor, Allah na iyayensu, yă zama alƙali tsakaninmu."

‡ **31:47** Kalman nan ta Yegar Sahaduta a Arameyanci yana nufin tsibi. § **31:47** Kalman nan da Ibraniyanci tana nufin tsibi. * **31:49** Mizfa yana nufin hasumiyar tsaro.

Saboda haka Yaƙub ya yi rantsuwa da sunan Tsoron mahaifinsa Ishaku. 54 Ya miƙa
hadaya a can a ƙasar tudu, ya kuma gayyaci danginsa zuwa wurin cin abinci. Bayan
suka ci, sai suka kwana a can.
55 Da sassafe kashegari sai Laban ya sumbaci jikokinsa da 'ya'yansa mata, ya sa
musu albarka. Sa'an nan ya yi bankwana da su, ya koma gida.

# 32

*Yaƙub ya shirya yǎ sadu da Isuwa*

1 Yaƙub shi ma ya kama hanyarsa, sai mala'ikun Allah suka sadu da shi. 2 Sa'ad
da Yaƙub ya gan su sai ya ce, "Wannan sansanin Allah ne!" Saboda haka ya kira
wannan wuri Mahanayim.*
3 Sai Yaƙub ya aiki manzanni su sha gabansa zuwa wurin ɗan'uwansa Isuwa a
ƙasar Seyir, a ƙauyen Edom. 4 Ya umarce su, "Ga abin da za ku faɗa wa maigidana
Isuwa, 'Bawanka Yaƙub ya ce, na yi zama tare da Laban na kuwa kasance a can sai
yanzu. 5 Ina da shanu da jakuna, tumaki da awaki, bayi maza da mata. Yanzu ina
aika da wannan saƙo zuwa ga ranka yǎ daɗe, don in sami tagomashi a idanunka.' "
6 Sa'ad da manzannin suka komo wurin Yaƙub, suka ce, "Mun tafi wurin
ɗan'uwanka Isuwa, yanzu kuwa yana zuwa ya sadu da kai, da kuma mutum ɗari
huɗu tare da shi."
7 Da tsoro mai yawa da kuma damuwa, Yaƙub ya rarraba mutanen da suke tare
da shi ƙungiyoyi† biyu, haka ma garkunan tumaki da awaki, da garkunan shanu da
raƙuma. 8 Ya yi tunani, "In Isuwa ya zo ya fāɗa wa ƙungiya ɗaya,‡ sai ƙungiya ɗayan
da ta ragu ta tsira."
9 Sa'an nan Yaƙub ya yi addu'a, "Ya Allah na mahaifina Ibrahim, Allah na mahaifina
Ishaku. Ya UBANGIJI kai da ka ce mini, 'Koma ƙasarka zuwa wurin danginka, zan
kuma sa ka yi albarka.' 10 Ban cancanci dukan alheri da amincin da ka nuna wa
bawanka ba. Da sanda kaɗai nake sa'ad da na ƙetare wannan Urdun, amma ga shi
yanzu na zama ƙungiyoyi biyu. 11 Ka cece ni, ina roƙonka daga hannun ɗan'uwana
Isuwa, gama ina tsoro zai zo yǎ fāɗa mini, yǎ karkashe mu duka, 'ya'ya da iyaye.
12 Amma ka riga ka faɗa, 'Tabbatacce zan sa ka yi albarka. Zan kuma sa zuriyarka
su zama kamar yashin teku da ba a iya ƙirgawa.' "
13 Ya kwana a can, daga cikin abin da yake tare da shi kuwa, ya zaɓi kyauta domin
ɗan'uwansa Isuwa, 14 awaki ɗari biyu da bunsurai ashirin, tumaki ɗari biyu da
raguna ashirin, 15 raƙuma mata talatin tare da ƙanānansu, shanu arba'in da bijimai
goma, jakuna mata ashirin da kuma jakuna maza goma. 16 Ya sa su a ƙarƙashin
kulawar bayinsa, kowane kashin garke ya kasance a ware. Ya ce wa bayinsa, "Ku sha
gabana, ku kuma ba da rata tsakanin garke da garke."
17 Ya umarci wanda yake jagorar ya ce, "Sa'ad da ɗan'uwana Isuwa ya sadu da ku
ya kuma yi tambaya, 'Ku na wane ne, ina za ku, kuma wane ne mai dukan dabbobin
nan da suke gabanku?' 18 Sai ku ce, 'Na bawanka Yaƙub ne. Kyauta ce wa maigidana
Isuwa, yana kuma tafe a bayanmu.' "
19 Yaƙub ya kuma umarci na biyu da na uku da kuma dukan waɗansu da suka
bi garkunan, "Sai ku faɗa irin abu guda ga Isuwa sa'ad da kuka sadu da shi. 20 Ku
kuma tabbata kun ce, 'Bawanka Yaƙub yana tafe a bayanmu.' " Gama Yaƙub ya yi
tunani cewa, "Zan kwantar da ran Isuwa da waɗannan kyautai, kafin mu sadu fuska
da fuska, wataƙila yǎ karɓe shi." 21 Saboda haka kyautai Yaƙub suka sha gabansa,
amma shi kansa ya kwana a sansani.

* 32:2 Mahanayim yana nufin sansanoni biyu. † 32:7 Ko kuwa sansanoni; haka ma a aya 10 ‡ 32:8 Ko
kuwa sansani

### *Yaƙub ya yi kokawa da Allah*

22 A wannan dare Yaƙub ya tashi ya ɗauki matansa biyu, da matan nan biyu masu
hidima da ʼyaʼyansa goma sha ɗaya ya haye rafin Yabbok. 23 Bayan ya sa suka haye
rafin, haka ma ya tura dukan mallakarsa zuwa hayen. 24 Saboda haka sai aka bar
Yaƙub shi kaɗai. Sai ga wani mutum ya zo ya yi kokawa da shi har wayewar gari.
25 Da mutumin ya ga cewa bai fi ƙarfin Yaƙub ba, sai ya bugi kwarin ƙashin cinyar
Yaƙub, sai gaɓar ƙashin cinyarsa ya goce, a saʼad da yake kokawa da mutumin.
26 Saʼan nan mutumin ya ce, "Bar ni in tafi, gama gari ya waye."

Amma Yaƙub ya amsa ya ce, "Ba zan bar ka ka tafi ba, sai ka sa mini albarka."

27 Mutumin ya tambaye shi ya ce, "Mene ne sunanka?"

Yaƙub ya amsa ya ce, "Yaƙub."

28 Sai mutumin ya ce, "Sunanka ba zai ƙara zama Yaƙub ba, amma Israʼila,§ gama
ka yi kokawa da Allah da mutane, ka kuwa yi rinjaye."

29 Yaƙub ya ce, "Ina roƙonka, faɗa mini sunanka."

Amma mutumin ya amsa ya ce, "Me ya sa kake tambayata sunana?" Saʼan nan ya
albarkace shi.

30 Saboda haka Yaƙub ya kira wurin Feniyel,* yana cewa, "Domin na ga Allah fuska
da fuska, duk da haka aka bar ni da rai."

31 Rana ta yi sama a saʼad da ya wuce Fenuwel yana kuma ɗingishi saboda ƙashin
cinyarsa. 32 Wannan ya sa har wa yau Israʼilawa ba sa cin jijiyar ƙashin cinya wadda
take a kwarin ƙashin cinya, domin an taɓa kwarin ƙashin cinyar Yaƙub kusa da
jijiyar.

# 33

### *Yaƙub ya sadu da Isuwa*

1 Yaƙub ya ɗaga ido ke nan, sai ga Isuwa yana zuwa tare da mutanensa ɗari huɗu;
saboda haka sai ya rarraba ʼyaʼyan wa Liyatu, Rahila da kuma matan nan biyu masu
hidima. 2 Ya sa matan nan biyu masu hidima da ʼyaʼyansu a gaba, Liyatu da ʼyaʼyanta
biye, saʼan nan Rahila da Yusuf a baya. 3 Shi kansa ya sha gabansu, ya rusuna har
ƙasa sau bakwai, kafin ya kai kusa da inda ɗanʼuwansa Isuwa yake.

4 Amma Isuwa ya ruga a guje ya sadu da Yaƙub ya rungume shi; ya faɗa a wuyansa
ya sumbace shi. Suka kuma yi kuka. 5 Saʼan nan Isuwa ya ɗaga ido ya ga mata da
ʼyaʼya. Ya yi tambaya, "Su wane ne waɗannan tare da kai?"

Yaƙub ya amsa, "Su ne ʼyaʼyan da Allah cikin alheri ya ba bawanka."

6 Sai matan nan biyu masu hidima da ʼyaʼyansu suka matso kusa suka durƙusa.
7 Biye da su, Liyatu da ʼyaʼyanta suka zo suka rusuna. A ƙarshe duka, sai Yusuf da
Rahila suka zo, su ma suka rusuna.

8 Isuwa ya yi tambaya, "Me kake nufi da dukan abubuwan nan da na sadu da su
ana korarsu?"

Sai Yaƙub ya ce, "Don in sami tagomashi a idanunka ne, ranka yă daɗe."

9 Amma Isuwa ya ce, "Na riga na sami abin da ya ishe ni, ɗanʼuwana. Riƙe abin
da kake da shi don kanka."

10 Sai Yaƙub ya ce, "Aʼa, ina roƙonka, in na sami tagomashi a idanunka, sai ka
karɓi wannan kyautai daga gare ni. Gama ganin fuskarka kamar ganin fuskar Allah
ne, yanzu da ka karɓe ni da farin ciki. 11 Ina roƙonka ka karɓi kyautar da aka kawo
maka, gama Allah ya yi mini alheri kuma ina da kome da nake bukata." Ganin yadda
Yaƙub ya nace, sai Isuwa ya karɓa.

12 Saʼan nan Isuwa ya ce, "Bari mu tafi, zan yi maka rakiya."

---

§ **32:28** Israʼila yana nufin ya yi kokawa da Allah. * **32:30** Feniyel yana nufin fuskar Allah.

[13] Amma Yaƙub ya ce masa, “Ranka yă daɗe, ka san cewa ’ya’yan ƙanana ne, dole
in lura da tumaki da shanun da suke shayar da jariransu. In aka kore su da gaggawa
a rana guda kaɗai, dukan dabbobin za su mutu. [14] Saboda haka bari ranka yă daɗe
yă sha gaban bawansa, ni kuma in tafi a hankali bisa ga saurin abin da ake kora a
gabana da kuma saurin ’ya’yan, sai na iso wurinka ranka yă daɗe, a Seyir.”
[15] Sai Isuwa ya ce, “To, bari in bar waɗansu mutanena tare da kai.”
Yaƙub ya ce, “Amma me ya sa za ka yi haka? Bari dai in sami tagomashi a idanunka
ranka yă daɗe.”
[16] Saboda haka a wannan rana Isuwa ya kama hanyar komawa zuwa Seyir. [17] Yaƙub
kuwa, ya tafi Sukkot, inda ya gina wuri domin kansa, ya kuma yi bukkoki domin
dabbobinsa. Shi ya sa aka kira wurin Sukkot.*
[18] Bayan Yaƙub ya zo daga Faddan Aram,† ya iso lafiya a birnin‡ Shekem a Kan’ana,
ya kuma kafa sansani a ƙofar birni. [19] Ya sayi fili daga ’ya’yan Hamor maza, mahaifin
Shekem inda ya kafa tentinsa, a bakin azurfa§ ɗari. [20] A can ya kafa bagade ya kuma
kira shi El Elohe Isra’ila.*

# 34

*Dina da mutanen Shekem*

[1] To, Dina, ’yar da Liyatu ta haifa wa Yaƙub, ta je ta ziyarci matan ƙasar. [2] Sa’ad
da Shekem ɗan Hamor Bahiwiye mai mulkin wurin ya gan ta, sai ya kama ta, ya
kwana da ita, ya ɓata ta. [3] Zuciyarsa kuwa ta damu da son Dina ’yar Yaƙub, ya kuwa
ƙaunaci yarinyar, ya yi mata magana a hankali. [4] Sai Shekem ya ce wa mahaifinsa
Hamor, “Ka auro mini wannan yarinya ta zama matata.”
[5] Sa’ad da Yaƙub ya ji cewa an ɓata ’yarsa Dina, sai ya yi shiru game da batun sai
’ya’yansa maza sun dawo gida, gama ’ya’yansa suna a jeji tare da dabbobinsa suna
kiwo.
[6] Sai Hamor mahaifin Shekem ya je don yă yi magana da Yaƙub. [7] Da ’ya’yan
Yaƙub maza suka dawo daga jeji sai suka ji labarin. Abin kuwa ya zafe su ƙwarai,
don Shekem ya jawo abin kunya wa jama’ar Isra’ila ta wurin kwana da ’yar Yaƙub,
don bai kamata wannan abu yă faru ba.
[8] Amma Hamor ya ce musu, “Dana Shekem ya sa zuciyarsa a kan ’yarku. Ina
roƙonku ku ba shi ita yă aura. [9] Ku yi auratayya da mu; ku aurar mana da ’ya’yanku
mata, ku kuma ku auro ’ya’yanmu mata wa kanku. [10] Za ku iya zauna a cikinmu,
ƙasar tana nan a buɗe dominku. Ku yi zama a cikinta, ku yi sana’a,* ku kuma sami
dukiya.”
[11] Sai Shekem ya ce wa mahaifin Dina da kuma ’yan’uwanta. “Bari in sami
tagomashi a idanunku, zan kuwa ba ku duk abin da kuka tambaya. [12] Ku faɗa mini
nawa ne dukiyar aure da kuma sadakin da zan kawo bisa ga yadda kuke so, zan
kuwa biya duk abin da kuka ce. Ku dai bar ni in aure yarinyar ta zama matata.”
[13] Domin an ɓata ’yar’uwansu Dina, sai ’ya’yan Yaƙub maza suka amsa a ha’ince
yayinda suke wa Shekem da mahaifinsa Hamor magana. [14] Suka ce musu, “Ba za
mu iya yin wannan abu ba, ba za mu iya ba da ’yar’uwarmu ga mutumin da ba
shi da kaciya ba. Wannan zai zama abin kunya ne a gare mu. [15] Za mu yarda da
wannan kaɗai ta wannan sharaɗi, cewa za ku zama kamar mu ta wurin yin wa
dukan ’ya’yanku maza kaciya. [16] Sa’an nan za mu ba da ’ya’yanmu mata aure gare

---

* **33:17** Sukkot yana nufin bukkoki. † **33:18** Wato, arewa maso yammancin Mesofotamiya ‡ **33:18** Ko kuwa isa a Salem, wani § **33:19** Da Ibraniyanci Kesita ɗari; Kesita shi ne ma’aunin kuɗi na nauyi da kuma darajar abin da ba a sani ba. * **33:20** El Elohe Isra’ila yana nufin Allah, Allahn Isra’ila ko kuwa Maɗaukaki ne Allah na Isra’ila. * **34:10** Ko kuwa ku yi ma’amala a sauƙaƙe; haka ma a aya 21

ku, mu kuma mu aure ʼyaʼyanku mata wa kanmu. Za mu zauna a cikinku mu kuma
zama mutane ɗaya da ku. 17 Amma in ba za ku yarda a yi muku kaciya ba, za mu
ɗauki ʼyarʼuwanmu† mu tafi.”

18 Sharuɗansu sun gamshi Hamor da ɗansa, Shekem. 19 Saurayin wanda aka fi
girmamawa a cikin dukan gidan mahaifinsa, bai ɓata lokaci a yin abin da suka ce
ba, domin ya ji daɗin ʼyar Yaƙub. 20 Saboda haka Hamor da ɗansa Shekem suka
tafi ƙofar birninsu don su yi magana da mutanen garinsu. 21 Suka ce, “Waɗannan
mutane ba su da damuwa, bari su zauna a cikin ƙasarmu, su kuma yi sanaʼa a ciki;
ƙasar tana da isashen fili dominsu. Za mu iya auro ʼyaʼyansu mata, su kuma su auri
namu. 22 Amma mutanen za su yarda su zauna tare da mu kamar mutane ɗaya kawai
bisa wannan sharaɗi, cewa a yi wa mazanmu kaciya, kamar yadda su kansu suke.
23 Ashe, shanunsu, dukiyarsu da dukan sauran dabbobinsu, ba za su zama namu ba?
Saboda haka mu yarda, za su kuwa zauna a cikinmu.”

24 Dukan mazan da suka fito ƙofar birnin suka yarda da Hamor da kuma ɗansa
Shekem, aka kuwa yi wa kowane namiji a birnin kaciya.

25 Bayan kwana uku, yayinda dukansu suna cikin zafi mikin kaciya, sai biyu daga
cikin ʼyaʼyan Yaƙub maza, Simeyon da Lawi, ʼyanʼuwan Dina, suka ɗauki takubansu
suka fāɗa wa birnin ba labari, suka kashe kowane namiji. 26 Suka kashe Hamor da
ɗansa Shekem da takobi, suka ɗauko Dina daga gidan Shekem suka tafi. 27 Saʼan nan
ʼyaʼyan Yaƙub maza suka bi kan gawawwakin, suka washe arzikin birni‡ saboda an
ɓata ʼyarʼuwarsu. 28 Suka kwashe garkunansu na shanu da jakuna, da kuma kome na
mutanen a birnin da kuma cikin gonaki. 29 Suka kwashe dukan dukiyarsu da dukan
matansu da ʼyaʼyansu, suka kwashe kome da yake cikin gidaje.

30 Sai Yaƙub ya ce wa Simeyon da Lawi, “Kun jawo mini wahala ta wurin sa in
zama abin ƙi ga Kanʼaniyawa da Ferizziyawa, mazaunan wannan ƙasa. Mu kima ne,
in kuwa suka haɗa kai gāba da ni, suka fāɗa mini, za su hallaka ni da gidana.”

31 Amma ʼyaʼyansa suka amsa, “To§, ya dace ke nan da ya yi da ʼyarʼuwarmu kamar
karuwa?”

# 35

*Yaƙub ya koma zuwa Betel*

1 Saʼan nan Allah ya ce wa Yaƙub, “Haura zuwa Betel ka yi zama a can, ka kuma
gina bagade a can wa Allah wanda ya bayyana gare ka saʼad da kake gudu daga
ɗanʼuwanka Isuwa.”

2 Saboda haka Yaƙub ya ce wa gidansa da kuma dukan waɗanda suke tare da
shi, “Ku zubar da baƙin allolin da kuke da su, ku tsarkake kanku, ku kuma canja
tufafinku. 3 Saʼan nan ku zo, mu haura zuwa Betel, inda zan gina bagade wa Allah
wanda ya amsa mini a ranar wahalata, wanda kuma ya kasance tare da ni a dukan
inda na tafi.” 4 Saboda haka suka ba Yaƙub dukan baƙin allolin da suke da su, da
zoban da suke kunnuwansu, sai Yaƙub ya binne su a ƙarƙashin itacen oak a Shekem.
5 Saʼan nan suka kama hanya, tsoron Allah kuwa ya kama dukan garuruwan da suke
kewayensu har babu wanda ya iya bin su.

6 Yaƙub da dukan mutanen da suke tare da shi suka zo Luz (wato, Betel) a ƙasar
Kanʼana. 7 A can ya gina bagade, ya kuma kira wurin El Betel,* gama a can ne Allah
ya bayyana kansa gare shi saʼad da yake gudu daga ɗanʼuwansa.

8 To, Debora, ungozomar Rebeka ta rasu aka kuma binne ta a ƙarƙashin itacen oak,
ƙasa da Betel. Saboda haka aka kira wurin Allon Bakut.†

† **34:17** Da Ibraniyanci ʼya. ‡ **34:27** Ko kuwa domin § **34:31** Ko kuwa wato * **35:7** El Betel yana nufin Allah na Betel. † **35:8** Allon yana nufin itacen oak na kuka.

9 Bayan Yaƙub ya komo daga Faddan Aram,‡ sai Allah ya bayyana gare shi, ya kuma
albarkace shi. 10 Allah ya ce masa, “Sunanka Yaƙub§ ne, amma ba za a ƙara kira ka
Yaƙub ba; sunanka zai zama Isra’ila.”* Saboda haka ya ba shi suna Isra’ila.
11 Sai Allah ya ce masa, “Ni ne Allah Maɗaukaki†, ka yi ta haihuwa, ka kuma
riɓaɓɓanya. Al’umma da tarin al’ummai za su fito daga gare ka, sarakuna kuma
za su fito daga jikinka. 12 Kasar da na ba wa Ibrahim da Ishaku, zan kuma ba ka, zan
kuma ba da wannan ƙasa ga zuriyarka a bayanka.” 13 Sa’an nan Allah ya tashi sama
daga gare shi a wurin da ya yi magana da shi.
14 Yaƙub kuwa ya kafa al’amudin dutse a inda Allah ya yi magana da shi, ya zuba
hadaya ta sha a kansa; ya kuma zuba mai a kansa. 15 Yaƙub ya kira inda Allah ya yi
magana da shi, Betel.‡

### *Mutuwar Rahila da Ishaku*

16 Sa’an nan suka tashi daga Betel. Yayinda suna da ɗan nisa da Efrat, sai Rahila
ta fara naƙuda ta kuwa sha wahala sosai. 17 Sa’ad da take cikin zafin haihuwa, sai
macen da ta karɓi haihuwar ta ce mata, “Kada ki ji tsoro, gama yanzu kin sami wani
ɗa.” 18 Yayinda take jan numfashinta na ƙarshe, sai ta ba wa ɗanta suna Ben-Oni.§
Amma mahaifinsa ya kira shi Benyamin.*
19 Ta haka Rahila ta rasu, aka kuma binne ta a hanya zuwa Efrata (wato, Betlehem).
20 Yaƙub ya kafa al’amudi bisa kabarinta, al’amudin kabarin Rahila ke nan, wanda
yake can har wa yau.
21 Isra’ila ya yi gaba, ya kafa tentinsa gaba da Migdal Eder. 22 Yayinda Isra’ila yana
zama a wancan yanki, Ruben ya shiga ya kwana da Bilha ƙwarƙwarar mahaifinsa,
Isra’ila kuwa ya ji labari.

Yaƙub ya haifi ’ya’ya maza goma sha biyu.

23 ’Ya’yan Liyatu maza,
Ruben shi ne ɗan fari na Yaƙub.
Sauran su ne, Simeyon, Lawi, Yahuda, Issakar da Zebulun.
24 ’Ya’yan Rahila maza su ne,
Yusuf da Benyamin.
25 ’Ya’yan Bilha maza, mai hidimar Rahila su ne,
Dan da Naftali.
26 ’Ya’yan Zilfa maza, mai hidimar Liyatu su ne,
Gad da Asher.

Waɗannan su ne ’ya’yan Yaƙub maza, waɗanda aka haifa masa a Faddan Aram.

27 Yaƙub ya dawo gida wurin mahaifinsa Ishaku a Mamre, kusa da Kiriyat Arba
(wato, Hebron), inda Ibrahim da Ishaku suka zauna. 28 Ishaku ya rayu shekaru ɗari
da tamanin, 29 sa’an nan ya ja numfashinsa na ƙarshe, ya kuwa mutu, aka kuma tara
shi ga mutanensa da kyakkyawan tsufa da kuma cikakken shekaru. ’Ya’yansa maza,
Isuwa da Yaƙub suka binne shi.

‡ **35:9** Wato, arewa maso yammancin Mesofotamiya, haka ma a aya 26 § **35:10** Yaƙub yana nufin ya kama ɗiɗɗige, a habaici dai, ya ruɗi. * **35:10** Isra’ila yana nufin kokawa da Allah. † **35:11** Da Ibraniyanci El-Shaddai ‡ **35:15** Betel yana nufin gidan Allah. § **35:18** Ben-Oni yana nufin ɗa na wahalata. * **35:18** Benyamin yana nufin ɗa na hannun damana.

# 36

*Zuriyar Isuwa*

1 Waɗannan su ne zuriyar Isuwa (wato, Edom).

2 Isuwa ya ɗauko matansa daga cikin matan Kan'ana, ya ɗauko Ada 'yar Elon
mutumin Hitti, da Oholibama 'yar Ana wadda take jikanyar Zibeyon Bahiwiye 3 ya
kuma auri Basemat 'yar Ishmayel wadda take 'yar'uwar Nebayiwot.
4 Ada ta haifi wa Isuwa, Elifaz. Basemat kuma ta haifa masa Reyuwel. 5 Oholibama
kuwa ta haifa masa Yewush, Yalam da Kora. Waɗannan su ne 'ya'yan Isuwa maza,
waɗanda aka haifa masa a Kan'ana.
6 Isuwa ya ɗauki matansa da 'ya'yansa maza da mata da kuma dukan membobin
gidansa, ya kuma ɗauki shanunsa da dukan sauran dabbobinsa, da dukan dukiyarsa
da ya samu a ƙasar Kan'ana zuwa wata ƙasa nesa da ɗan'uwansa Yaƙub.
7 Mallakarsu ta yi yawa ƙwarai da ba za su iya zauna tare ba; gama ƙasar da suke
zaune a ciki ba za tă ishe su su biyu ba saboda dabbobinsu. 8 Saboda haka Isuwa
(wato, Edom) ya zauna a ƙasar tuddai na Seyir.

9 Wannan shi ne zuriyar Isuwa, kakan mutanen Edom, a ƙasar tuddai na Seyir.

10 Waɗannan su ne sunayen 'ya'yan Isuwa maza,
Elifaz, ɗan Ada matar Isuwa, da Reyuwel ɗan Basemat matar Isuwa.
11 'Ya'yan Elifaz maza su ne,
Teman, Omar, Zefo, Gatam da Kenaz. 12 Elifaz ɗan Isuwa kuma yana da
ƙwarƙwara mai suna Timna, wadda ta haifa masa Amalek. Waɗannan su ne jikokin Ada matar Isuwa.
13 'Ya'yan Reyuwel maza su ne,
Nahat, Zera, Shamma da Mizza. Waɗannan su ne jikokin Basemat matar Isuwa.
14 'Ya'yan Oholibama maza 'yar Ana wadda take jikanyar Zibeyon, matar Isuwa, waɗanda ta haifa wa Isuwa su ne,
Yewush, Yalam da Kora.

15 Waɗannan su ne manya a cikin zuriyar Isuwa,
'Ya'ya Elifaz maza ɗan farin Isuwa,
Shugabannin su ne; Teman, Omar, Zefo, Kenaz, 16 Kora,* Gatam da kuma Amalek.
Waɗannan ne manya da suka fito daga dangin Elifaz a Edom; su ne jikokin Ada.
17 'Ya'yan Reyuwel maza,
Shugabannin su ne; Nahat, Zera, Shamma da Mizza. Waɗannan su ne manya da suka fito daga dangin Reyuwel a Edom; su ne jikokin Basemat matar Isuwa.
18 'Ya'yan Oholibama maza matar Isuwa,
Shugabannin su ne; Yewush, Yalam da Kora. Waɗannan su ne manya da suka fito daga dangin Oholibama 'yar Ana matar Isuwa.
19 Waɗannan su ne 'ya'yan Isuwa maza (wato, Edom), waɗannan ne manyansu.

20 Waɗannan su ne 'ya'yan Seyir Bahore maza, waɗanda suke zaune a yankin,
Lotan, Shobal, Zibeyon, Ana, 21 Dishon, Ezer da Dishan. Waɗannan su ne manyan Horiyawa, 'ya'yan Seyir, maza, a ƙasar Edom.
22 'Ya'yan Lotan maza su ne,

* **36:16** Masoretik, Fentatut na Samariya (dubi kuma Far 36.11 da 2Tar 1.3-6) ba su da Kora.

Hori da Homam.† Timna ’yar’uwar Lotan ce.
23 ’Ya’yan Shobal maza su ne,
Alwan, Manahat, Ebal, Shefo da Onam.
24 ’Ya’yan Zibeyon maza su ne,
Aiya da Ana. Wannan shi ne Ana wanda ya sami maɓulɓulan‡ ruwan zafi a hamada yayinda yake kiwon jakuna na mahaifinsa Zibeyon.
25 ’Ya’yan Ana su ne,
Dishon da Oholibama ’yar Ana.
26 ’Ya’yan Dishon maza§ su ne,
Hemdan, Eshban, Itran da Keran.
27 ’Ya’yan Ezer maza su ne,
Bilhan, Za’aban da Akan.
28 ’Ya’yan Dishan maza su ne,
Uz da Aran.
29 Waɗannan su ne manyan Horiyawa,
Lotan, Shobal, Zibeyon, Ana,
30 Dishon, Ezer da Dishan.
Waɗannan su ne manyan Horiyawa, bisa ga ɓangarorinsu, a ƙasar Seyir.

### *Masu mulkin Edom*

31 Waɗannan su ne sarakunan da suka yi mulki a Edom kafin wani sarki mutumin Isra’ila yă yi mulki,*
32 Bela ɗan Beyor ya zama sarkin Edom. Sunan birninsa shi ne Dinhaba.
33 Sa’ad da Bela ya rasu, Yobab ɗan Zera daga Bozra ya gāje shi.
34 Sa’ad da Yobab ya rasu, Husham daga ƙasar Temaniyawa ya gāje shi.
35 Sa’ad da Husham ya rasu, Hadad ɗan Bedad, wanda ya ci Midiyan da yaƙi a ƙasar Mowab, ya gāje shi. Sunan birninsa shi ne Awit.
36 Sa’ad da Hadad ya rasu, Samla daga Masreka ya gāje shi.
37 Sa’ad da Samla ya rasu, Sha’ul daga Rehobot na ta kogi† ya gāje shi.
38 Sa’ad da Sha’ul ya rasu, Ba’al-Hanan ɗan Akbor ya gāje shi.
39 Sa’ad da Ba’al-Hanan ɗan Akbor ya rasu, Hadad‡ ya gāje shi. Sunan birninsa shi ne Fau, kuma sunan matarsa Mehetabel ce ’yar Matired, jikanyar Me-Zahab.

40 Waɗannan su ne manya da suka fito daga zuriyar Isuwa, bisa ga danginsu, bisa kuma ga kabilansu da yankunansu. Sunayensu su ne,
Timna, Alwa, Yetet.
41 Oholibama, Ela, Finon.
42 Kenaz, Teman, Mibzar.
43 Magdiyel da Iram.
Waɗannan su ne manyan Edom bisa ga mazauninsu cikin ƙasar da suka zauna.

Wannan shi ne zuriyar Isuwa, kakan mutanen Edom.

## 37

### *Mafarkan Yusuf*

1 Yaƙub ya zauna a ƙasar da mahaifinsa ya zauna, wato, ƙasar Kan’ana.

---

† **36:22** Da Ibraniyanci Hemam, wani suna na Homam (dubi 1Tar 1.39) ‡ **36:24** Bulget, Siriyak sami ruwa; ma’anar Ibraniyanci don wannan kalma ba tabbatacce ba ne. § **36:26** Da Ibraniyanci Dishan, wani suna na Dishon * **36:31** Ko kuwa kafin wani sarkin Isra’ilawa ya yi mulki a kansu † **36:37** Mai yiwuwa Yuferites ‡ **36:39** Yawancin rubuce-rubucen hannu na Masoretik, Fentatut na Samariya da Siriyak (dubi kuma 1Tar 1.50); yawancin rubuce-rubucen hannu na Masoretik suna da Hadar ne.

2 Wannan shi ne labarin zuriyar Yaƙub.

Yusuf, saurayi ne mai shekara goma sha bakwai. Shi da ’yan’uwansa, wato, ’ya’yan
Bilha maza da kuma ’ya’yan Zilfa maza, matan mahaifinsa suna kiwon garkuna tare.
Sai Yusuf ya kawo wa mahaifinsu rahoto marar kyau game da ’yan’uwansa.

3 Isra’ila dai ya fi ƙaunar Yusuf fiye da kowanne a cikin sauran ’ya’yansa maza,
gama an haifa masa shi a cikin tsufansa. Sai ya yi masa riga mai gwanin kyau.*
4 Sa’ad da ’yan’uwansa suka ga cewa mahaifinsu ya fi ƙaunarsa fiye da kowanne
daga cikinsu, sai suka ƙi jininsa, ba sa kuma maganar alheri da shi.

5 Sai Yusuf ya yi mafarki, sa’ad da ya faɗa wa ’yan’uwansa, suka ƙara ƙin jininsa.
6 Ya ce musu, “Ku saurari wannan mafarkin da na yi. 7 Muna daurin dammunan
hatsi a gona, sai nan da nan damina ya tashi ya tsaya, yayinda dammunanku suka
taru kewaye da nawa suka rusuna masa.”

8 Sai ’yan’uwansa suka ce masa, “Kana nufin za ka yi mulki a kanmu ke nan? Ko
kuwa za ka zama sarki, a bisanmu?” Suka ƙara ƙin jininsa saboda mafarkinsa da
kuma abin da ya faɗa.

9 Sai Yusuf ya sāke yin wani mafarki, ya faɗa wa ’yan’uwansa. Ya ce, “Ku saurara,
na sāke yin wani mafarki, a wannan lokaci, na ga rana da wata da taurari goma sha
ɗaya suna rusuna mini.”

10 Sa’ad da ya faɗa wa mahaifinsa da kuma ’yan’uwansa, sai mahaifinsa ya kwaɓe
shi ya ce, “Wanne irin mafarki ne haka da ka yi? Kana nufin ni da mahaifiyarka da
’yan’uwanka za mu zo gabanka mu rusuna maka?” 11 ’Yan’uwansa suka yi kishinsa,
amma mahaifinsa ya riƙe batun nan a zuciya.

### *’Yan’uwan Yusuf maza sun sayar da shi*

12 To, ’yan’uwansa suka tafi kiwon garkunan mahaifinsu kusa da Shekem. 13 Sai
Isra’ila ya ce wa Yusuf, “Kamar yadda ka sani, ’yan’uwanka suna kiwon garkuna
kusa da Shekem. Zo, in aike ka gare su.”

Ya ce, “To.”

14 Saboda haka Isra’ila ya ce wa Yusuf, “Jeka ka ga ko kome lafiya yake da
’yan’uwanka da kuma garkunan, ka kawo mini labari.” Sa’an nan ya sallame shi
daga Kwarin Hebron.

Sa’ad da Yusuf ya kai Shekem, 15 sai wani mutum ya same shi yana yawo a cikin
jeji, sai mutumin ya tambaye shi ya ce, “Me kake nema?”

16 Yusuf ya amsa ya ce, “Ina neman ’yan’uwana ne. Za ka iya faɗa mini inda suke
kiwon garkunansu?”

17 Mutumin ya amsa, “Sun yi gaba daga nan. Na ji su suna cewa, ‘Bari mu je
Dotan.’ ”

Saboda haka Yusuf ya bi bayan ’yan’uwansa, ya kuwa same su kusa da Dotan.
18 Amma da suka gan shi daga nesa, kafin yă kai wurinsu, sai suka ƙulla su kashe shi.

19 Suka ce wa juna, “Ga mai mafarkin nan can zuwa! 20 Ku zo mu kashe shi mu
kuma jefa shi a ɗaya daga cikin rijiyoyin nan, mu ce mugun naman jeji ya cinye shi.
Mu ga yadda mafarkinsa zai cika.”

21 Sa’ad da Ruben ya ji wannan, sai ya yi ƙoƙari yă cece shi daga hannuwansu.
Ya ce, “Kada mu ɗauki ransa. 22 Kada mu zub da wani jini. Mu dai jefa shi cikin
wannan rijiya a nan cikin hamada, amma kada mu sa hannu a kansa.” Ruben ya
faɗa wannan ne don yă cece shi daga gare su, yă kuma mai da shi ga mahaifinsa.

* **37:3** Ma’anar Ibraniyanci na mai ado ba tabbatacce ba ne; haka ma a ayoyi 23 da 32.

23 Saboda haka sa'ad da Yusuf ya zo wurin 'yan'uwansa, sai suka tuɓe masa rigarsa,
rigan nan mai gwanin kyau da ya sa, 24 suka kuma ɗauke shi suka jefa a cikin rijiya.
To, rijiyar wofi ce, babu ruwa a ciki.

25 Da suka zauna don cin abinci, sai suka tā da idanu, suka ga ayarin mutanen
Ishmayel suna zuwa daga Gileyad. An yi wa raƙumansu labtu da kayan yaji da na
ƙanshi, suna kan hanyarsu za su Masar.

26 Yahuda ya ce wa 'yan'uwansa, "Me zai amfane mu in muka kashe ɗan'uwanmu
muka ɓoye jininsa? 27 Ku zo, mu sayar da shi wa mutanen Ishmayelawan nan, kada
mu sa hannuwanmu a kansa; ban da haka ma, shi ɗan'uwanmu ne, jiki da jininmu."
Sai 'yan'uwansa suka yarda.

28 Saboda haka sa'ad da Fataken Midiyawa suka iso, sai 'yan'uwansa suka ja Yusuf
daga rijiyar, suka sayar da shi a bakin shekel† ashirin na azurfa wa mutanen Ishmayel,
waɗanda suka ɗauke shi zuwa Masar.
29 Sa'ad da Ruben ya dawo wurin rijiyar, sai ya tarar cewa Yusuf ba ya can, sai ya
kyakkece tufafinsa. 30 Ya koma wurin 'yan'uwansa ya ce, "Yaron ba ya can! Ina zan
bi yanzu?"

31 Sai suka ɗauki rigar Yusuf, suka yanka akuya suka tsoma rigar a cikin jinin.
32 Suka ɗauki rigan nan mai gwanin kyau, suka kawo wa mahaifinsu suka ce, "Mun
sami wannan. Ka bincika shi ka gani ko rigar ɗanka ne."

33 Ya gane shi, sai ya ce, "Rigar ɗana ne! Waɗansu mugayen namun jeji sun cinye
shi. Tabbatacce an yayyaga Yusuf."

34 Sa'an nan Yaƙub ya kyakkece tufafinsa, ya sa tufafin makoki, ya kuma yi makoki
domin ɗansa kwanaki masu yawa. 35 Dukan 'ya'yansa maza da mata, suka zo don
su ta'azantar da shi, amma ya ƙi yă ta'azantu. Ya ce, "A'a, cikin makoki zan gangara
zuwa kabari‡ wurin ɗana." Saboda haka, mahaifin Yusuf ya yi kuka saboda shi.

36 Ana cikin haka, Midiyawa suka sayar da Yusuf a Masar wa Fotifar, ɗaya daga
cikin shugabannin 'yan gadin fadar Fir'auna.

# 38

*Yahuda da Tamar*

1 A wannan lokaci, Yahuda ya bar 'yan'uwansa ya gangara don yă zauna da
mutumin Adullam, mai suna Hira. 2 A can Yahuda ya sadu da 'yar wani Bakan'ane,
mai suna Shuwa. Ya aure ta, ya kuma kwana da ita; 3 ta yi ciki, ta kuma haifi ɗa,
wanda aka kira Er. 4 Ta sāke yin ciki, ta haifi wani ɗa, ta kira shi Onan. 5 Ta kuma
haifi wani ɗa har yanzu, aka kuwa ba shi suna Shela. A Kezib ne ta haife shi.

6 Sai Yahuda ya auro wa Er mata, ɗansa na fari, sunanta Tamar. 7 Amma Er, ɗan
farin Yahuda mugu ne a fuskar UBANGIJI, saboda haka UBANGIJI ya kashe shi.

8 Sa'an nan Yahuda ya ce wa Onan, "Ka kwana da matar ɗan'uwanka ka cika
wajibinka gare ta a matsayin ɗan'uwan miji, don ka samar wa ɗan'uwanka 'ya'ya."
9 Amma Onan ya san cewa 'ya'yan ba za su zama nasa ba; saboda haka a duk sa'ad
da ya kwana da matar ɗan'uwansa, sai yă zub da maniyyinsa a ƙasa don kada yă
samar wa ɗan'uwansa 'ya'ya. 10 Abin nan da ya yi mugunta ce a gaban UBANGIJI,
saboda haka UBANGIJI ya kashe shi, shi ma.

11 Sai Yahuda ya ce wa surukarsa Tamar, "Ki yi zama kamar gwauruwa a gidan
mahaifinki sai ɗana Shela ya yi girma." Gama ya yi tunani, "Shi ma zai mutu, kamar
'yan'uwansa." Saboda haka Tamar ta je ta zauna a gidan mahaifinta.

† **37:28** Wato, kamar ons 8 (kamar kilo 0.2) ‡ **37:35** Da Ibraniyanci Sheol.

12 Bayan an daɗe sai matar Yahuda, ʼyar Shuwa ta rasu. Saʼad da Yahuda ya gama
makoki, sai ya haura zuwa Timna, zuwa wurin mutanen da suke askin tumakinsa,
abokinsa Hira mutumin Adullam kuwa ya tafi tare da shi.
13 Saʼad da aka faɗa wa Tamar cewa, “Surukinki yana kan hanyarsa zuwa Timna
don askin tumakinsa,” 14 sai ta tuɓe rigunan gwaurancinta ta rufe kanta da lulluɓi
don ta ɓad da kamanninta, saʼan nan ta je ta zauna a ƙofar shigar Enayim, wadda
take a hanyar zuwa Timna. Gama ta lura cewa ko da yake Shela yanzu ya yi girma,
ba a ba da ita gare shi ta zama matarsa ba.
15 Saʼad da Yahuda ya gan ta, ya yi tsammani karuwa ce, gama ta lulluɓe fuskarta.
16 Bai san cewa ita surukarsa ce ba, sai ya ratse zuwa wurinta a gefen hanya ya ce,
“Zo mana, in kwana da ke.”
Sai ta ce, “Me za ka ba ni in na kwana da kai?”
17 Ya ce, “Zan aika miki da ɗan akuya daga garkena.”
Sai ta ce, “Za ka ba ni wani abu jingina, kafin ka aika da shi?”
18 Ya ce, “Wace jingina zan ba ki?”
Sai ta amsa, “Hatiminka da ka rataye a wuya da kuma sandan da yake a hannunka.”
Ya ba da su gare ta, ya kuma kwana da ita, sai ta yi ciki. 19 Bayan ta tafi, sai ta tuɓe
lulluɓin, ta sāke sa tufafin gwaurancinta.
20 Ana cikin haka sai Yahuda ya aika da ɗan akuya ta hannun abokinsa mutumin
Adullam don yă karɓo masa jinginar daga wurin macen, amma bai same ta a can ba.
21 Ya tambayi mutanen da suke zama a can ya ce, “Ina karuwar haikalin da take a
bakin hanya a Enayim?”
Sai suka ce, “Ba a taɓa kasance da karuwar haikali a nan ba.”
22 Saboda haka sai ya koma zuwa wurin Yahuda ya ce, “Ban same ta ba. Ban da
haka ma, mutanen da suke zama a can, sun ce, ‘Ba a taɓa kasance da wata karuwar
haikali a nan ba.’ ”
23 Saʼan nan Yahuda ya ce, “Bari tă riƙe kayan kiɗa garin nema mu zama abin
dariya. Ni kam, na aika da tunkiyar amma ba a same ta ba.”
24 Bayan misalin wata uku sai aka faɗa wa Yahuda cewa, “Tamar, surukarka ta yi
laifin karuwanci, a sakamakon haka yanzu ta yi ciki.”
Yahuda ya ce, “A fid da ita, a ƙone!”
25 Yayinda ake fitar da ita, sai ta aika saƙo zuwa wurin surukinta, ta ce, “Mutumin
da yake da waɗannan kayan ne ya yi mini ciki.” Ta kuma ƙara da cewa, “Duba ko
za ka gane da hatimin nan, da abin ɗamaran nan, da kuma sandan nan, ko na wane
ne?”
26 Yahuda ya gane su, sai ya ce, “Ai, ta fi ni gaskiya, da yake ban ba da ita ga ɗana
Shela ba.” Bai kuwa ƙara kwana da ita ba.
27 Saʼad da lokaci ya yi da za tă haihu, ashe, tagwaye ʼyan maza ne suke cikinta.
28 Yayinda take haihuwa, ɗaya daga cikinsu ya fid da hannunsa; sai ungonzomar ta
ɗauki jan zare ta ɗaura a hannun, ta ce, “Wannan ne ya fito da farko.” 29 Amma
saʼad da ya janye hannunsa, sai ɗanʼuwansa ya fito, sai ta ce, “Wato, haka ne ka keta
ka fito!” Sai aka ba shi suna Ferez.* 30 Saʼan nan ɗanʼuwansa wanda yake da jan
zare a hannunsa ya fito, aka kuma ba shi suna Zera.†

# 39

*Yusuf da matar Fotifar*

1 To, aka kai Yusuf Masar, Fotifar wani mutumin Masar wanda yake ɗaya daga
cikin hafsoshin Firʼauna, shugaban masu tsaro, ya saye shi daga mutanen Ishmayel
waɗanda suka kai shi can.

---

* **38:29** Ferez yana nufin ƙetawa waje. † **38:30** Zera na iya nufin ja ko mai haske.

2 Ubangiji kuwa yana tare da Yusuf, Yusuf kuwa yi nasara, ya zauna a gidan
mutumin Masar maigidansa. 3 Sa'ad da maigidansa ya ga cewa Ubangiji yana tare
da Yusuf, kuma cewa Ubangiji ya ba shi nasara a kome da ya yi, 4 sai Yusuf ya sami
tagomashi a idanunsa, ya kuma zama mai hidimarsa. Fotifar ya sa shi yă zama
shugaba a gidansa, ya kuma danƙa masa kome da yake da shi. 5 Daga lokacin da ya
sa shi shugaban gidansa da kuma a kan dukan abin da yake da shi, sai Ubangiji ya
albarkaci gidan mutumin Masar saboda Yusuf. Albarkar Ubangiji tana a kan kome da
Fotifar yake da shi a gida da kuma a jeji. 6 Saboda haka sai ya bar kome a ƙarƙashin
kulawar Yusuf, bai dame kansa a wani abu ba sai dai abincin da yake ci.

To, fa, Yusuf ƙaƙƙarfa ne, kyakkyawa kuma, 7 bayan an ɗan jima sai matar
maigidansa ta fara sha'awar Yusuf, sai ta ce, "Zo ka kwana da ni!"

8 Amma ya ƙi. Ya ce mata, "Ga shi kome yana a ƙarƙashina, don haka ne ma
maigidana bai dami kansa da wani abu a cikin gidan nan ba; kome da ya mallaka, ya
danƙa ga kulawata. 9 Babu wani da ya fi ni a wannan gida. Maigidana bai hana ni
kome ba sai ke, saboda ke matarsa ce. Yaya fa, zan yi irin wannan mugun abu, in yi
zunubi wa Allah?" 10 Ko da yake ta yi ta yin wa Yusuf maganar kowace rana, amma
ya ƙi yă kwana da ita, ko ma yă zauna da ita.

11 Wata rana, ya shiga cikin gida don yă yi ayyukansa, ba wani daga cikin bayin
gidan da yake ciki. 12 Sai ta cafke shi a riga, ta ce, "Zo ka kwana da ni!" Amma ya
bar rigarsa a hannunta, ya gudu ya fita daga gidan.

13 Sa'ad da ta ga ya bar rigarsa a hannunta ya gudu ya fita daga gidan, 14 sai ta kira
bayin gidan ta ce musu, "Duba, an kawo mana wannan mutumin Ibraniyawa don yă
ci mutuncinmu! Ya zo nan don yă kwana da ni, amma na yi ihu. 15 Sa'ad da ya ji na
yi ihu neman taimako, sai ya bar rigarsa kusa da ni, ya gudu ya fita daga gida."

16 Ta ajiye rigar kusa da ita sai da maigidansa ya dawo gida. 17 Sa'an nan ta faɗa
masa wannan labari, "Mutumin Ibraniyawan, bawan da ka kawo mana, ya zo wurina
don yă ci mutuncina. 18 Amma da zarar na yi ihu neman taimako, sai ya bar rigarsa
kusa da ni, ya gudu ya fita daga gida."

19 Sa'ad da maigidansa ya ji labarin da matarsa ta faɗa masa cewa, "Ga yadda
bawanka ya yi da ni," sai ya husata. 20 Maigidan Yusuf ya ɗauke shi ya sa a kurkuku,
wurin da ake tsare 'yan kurkukun sarki.

Amma yayinda Yusuf yake can a cikin kurkuku, 21 Ubangiji ya kasance tare da shi;
ya nuna masa alheri, ya kuma sa ya sami tagomashi a idanun mai gadin kurkukun.
22 Saboda haka mai gadin ya sa Yusuf ya zama shugaban dukan waɗanda aka tsare
a kurkukun, Yusuf ne kuma yake lura da dukan abin da ake yi a can. 23 Mai gadin ba
ya sa kansa game da kome da yake ƙarƙashin kulawar Yusuf, gama Ubangiji yana
tare da Yusuf, ya kuma ba shi nasara a cikin dukan abin da ya yi.

# 40

### *Mai riƙon kwaf da mai tuya*

1 Bayan ɗan lokaci, sai mai riƙon kwaf da mai tuyan sarkin Masar suka yi wa
maigidansu, sarkin Masar laifi. 2 Fir'auna ya yi fushi da hafsoshin nan nasa guda
biyu, shugaban masu shayarwa da shugaban masu tuya, 3 ya kuma sa su a kurkuku
a cikin gidan shugaban masu tsaro, a wannan kurkukun da aka sa Yusuf. 4 Sai
shugaban masu tsaro ya danƙa su a hannun Yusuf, ya kuwa yi musu hidima.

Bayan sun jima cikin kurkuku, 5 sai kowanne a cikin mutum biyun nan, mai riƙon
kwaf da mai tuya na sarkin Masar, waɗanda aka sa a kurkuku, suka yi mafarki a
dare ɗaya, kuma kowane mafarki ya kasance da fassara irin tasa.

6 Sa'ad da Yusuf ya zo wurinsu kashegari, sai ya ga duk sun damu. 7 Saboda haka ya
tambayi hafsoshin Fir'auna, waɗanda suke a kurkuku tare da shi, a gidan maigidansa
ya ce, "Me ya sa fuskokinku suke a ɓace haka?"
8 Sai suka amsa, "Mu biyu, mun yi mafarki, amma babu wani da zai fassara mana
su."
Sa'an nan Yusuf ya ce musu, "Fassara ba daga Allah take zuwa ba? Ku faɗa mini
mafarkanku."
9 Sai shugaban masu shayarwa ya faɗa wa Yusuf mafarkinsa. Ya ce masa, "A cikin
mafarkina, na ga kuringa a gabana, 10 kuma a kuringar, akwai rassa uku. Nan da
nan kuringar ta yi toho, ta huda, ta kuma yi nonna har suka nuna, suka zama inabi.
11 Kwaf Fir'auna kuwa yana a hannuna, na kuma ɗiba inabin na matse su cikin kwaf
Fir'auna, na kuma sa kwaf ɗin a hannunsa."
12 Yusuf ya ce masa, "Ga abin da mafarkin yake nufi, 'Rassan nan uku, kwana uku
ne. 13 Cikin kwana uku, Fir'auna zai fitar da kai, yǎ maido da kai a matsayinka, za
ka kuwa sa kwaf Fir'auna cikin hannunsa, kamar yadda ka saba yi sa'ad da kake
mai riƙon kwaf nasa. 14 Amma fa, sa'ad da kome ya zama maka da kyau, ka tuna
da ni, ka kuma yi mini alheri, ka ambace ni wa Fir'auna, ka fid da ni daga wannan
kurkuku. 15 Gama da ƙarfi ne aka ɗauke ni daga ƙasar Ibraniyawa, ko a nan ma ban
yi wani abin da ya cancanci a sa ni cikin kurkuku ba.' "
16 Sa'ad da shugaban masu tuya ya ga cewa Yusuf ya ba da fassara mai gamsarwa,
sai ya ce, wa Yusuf, "Ni ma na yi mafarki. A kaina, akwai kwanduna uku na burodi*.
17 A kwandon na bisa, akwai kayan iri-iri da aka toya, masu kyau domin Fir'auna,
amma tsuntsaye suka ci su a kwandon da yake kaina."
18 Yusuf ya ce, "Ga abin da mafarkin yake nufi, 'Kwanduna uku, kwanaki uku ne.
19 Cikin kwana uku, Fir'auna zai fid da kai, yǎ rataye ka a kan itace.† Tsuntsaye kuwa
za su ci naman jikinka.' "
20 To, a rana ta uku ne, ranar tunawa da haihuwar Fir'auna, ya kuwa yi biki wa
dukan hafsoshinsa. Ya fid da shugaban masu shayarwa da kuma shugaban masu
tuya a gaban hafsoshinsa. 21 Ya mai da shugaban masu shayarwa a matsayinsa,
saboda haka shugaban masu shayarwa ya sāke sa kwaf a hannun Fir'auna, 22 amma
ya rataye‡ shugaban masu tuya, kamar dai yadda Yusuf ya faɗa musu a fassarar
mafarkan da suka yi.
23 Shugaban masu shayarwa fa, bai tuna da Yusuf ba; ya mance da shi.

# 41

*Mafarkan Fir'auna*

1 Bayan shekaru biyu cif, Fir'auna ya yi mafarki. A mafarkin, ya ga yana tsaye kusa
da Nilu, 2 sai ga shanu bakwai masu ƙiba mulmul, suka fito daga kogin, suna kiwo
a cikin kyauro. 3 Bayansu, sai ga waɗansu shanu bakwai, munana, ramammu, suka
fito daga Nilu, suka tsaya kusa da waɗancan masu ƙiban, a bakin kogin. 4 Shanun
nan da suke munana ramammu, suka cinye shanu bakwai nan masu ƙiba mulmul.
Sai Fir'auna ya farka.
5 Ya sāke yin barci, sai ya yi mafarki na biyu; ya ga kawuna bakwai na dawa,
ƙosassu masu kyau, suka yi girma a kara guda. 6 Bayansu, sai ga waɗansu kawuna
bakwai na dawa, suka fito sirara waɗanda iskar gabas ta sa suka yanƙwane. 7 Siraran
dawan suka haɗiye kawuna bakwai nan ƙosassu masu kyau. Sai Fir'auna ya farka,
ashe, mafarki ne.

* **40:16** Ko kuwa kwanduna uku marasa ƙarfi † **40:19** Ko kuwa ya cira ka a itace ‡ **40:22** Ko kuwa cira

8 Da safe sai hankalinsa ya tashi, saboda haka sai ya aika a kawo dukan masu duba
da masu hikima na Masar. Fir'auna ya faɗa musu mafarkansa, amma babu wanda
ya iya ba shi fassararsu.

9 Sai shugaban masu shayarwa ya ce wa Fir'auna, "Yau an tuna mini da kāsawata.
10 Sai ya ci gaba ya ce, Fir'auna ya taɓa husata da bayinsa, ya kuma jefa ni da
shugaban masu tuya a cikin kurkuku a gidan shugaban masu tsaro. 11 Kowannenmu
ya yi mafarki a wani dare, kowane mafarki kuma ya kasance da ma'anarsa. 12 To,
wani saurayi, mutumin Ibraniyawa ya kasance a can tare da mu, bawan shugaban
masu tsaro. Sai muka faɗa masa mafarkanmu, ya kuwa fassara mana su, yana ba wa
kowane mutum fassarar mafarkinsa. 13 Abubuwan kuwa suka kasance daidai yadda
ya fassara su gare mu; aka mai da ni a matsayina, ɗaya mutumin kuwa aka rataye
shi."

14 Sai Fir'auna ya aika a kawo Yusuf, aka kuwa kawo shi da sauri daga kurkuku.
Sa'ad da ya yi aski, ya kuma canja tufafinsa, sai ya zo gaban Fir'auna.

15 Fir'auna ya ce wa Yusuf, "Na yi mafarki, kuma babu wanda ya iya fassara shi.
Amma na ji an ce sa'ad da ka ji mafarki, kana iya fassara shi."

16 Yusuf ya amsa wa Fir'auna ya ce, "Ba ni ne da iyawar ba, Allah zai iya ba wa
Fir'auna amsar da yake nema."

17 Sa'an nan Fir'auna ya ce wa Yusuf, "A cikin mafarkina, na ga ina tsaye a
bakin Nilu, 18 sai ga shanu bakwai masu ƙiba mulmul, suka fito daga kogin, suna
kiwo a cikin kyauro. 19 Bayansu kuma, sai ga waɗansu shanu bakwai suka fito
ƙanjamammu, munana, ramammu. Ban taɓa ganin irin munanan shanu haka a
cikin dukan ƙasar Masar ba. 20 Ramammun shanun nan munana, suka cinye shanun
nan bakwai masu ƙiba da suka fito da fari. 21 Amma ko bayan da suka cinye su, babu
wanda zai iya faɗa cewa sun yi haka; suna nan dai munana kamar yadda suke a dā.
Sai na farka.

22 "Har yanzu kuma, a cikin mafarkina na ga kawuna bakwai na dawa ƙosassu
masu kyau, suna girma a kara guda. 23 Bayansu, sai ga waɗansu kawuna bakwai suka
fito, yanƙwananne sirara waɗanda iskar gabas ta yanƙwane. 24 Siraran kawunan
dawan nan suka haɗiye kawuna bakwai nan masu kyau. Na faɗa wannan wa masu
duba, amma ba wanda ya iya fassara mini shi."

25 Sai Yusuf ya ce wa Fir'auna, "Mafarkan Fir'auna, ɗaya ne. Allah ya bayyana
wa Fir'auna abin da yake shirin yi. 26 Shanu masu kyau nan, shekaru bakwai ne,
kawunan dawa bakwai ƙosassun nan kuwa shekaru bakwai ne; mafarkan iri ɗaya
ne. 27 Shanun nan ramammu, munana, da suka zo daga baya, shekaru bakwai ne,
haka ma kawuna dawan nan shanyayyu da iskar gabas ta yanƙwane. Shekaru ne
bakwai na yunwa.

28 "Haka yake kamar yadda na faɗa wa Fir'auna cewa Allah ya nuna wa Fir'auna
abin da yake shirin yi. 29 Shekaru bakwai na yalwar abinci suna zuwa a dukan ƙasar
Masar, 30 amma shekaru bakwai na yunwa za su biyo bayansu. Tsananin yunwar za
tă sa a manta da dukan isashen abincin da aka samu a ƙasar Masar, yunwa kuwa
za tă rufe dukan ƙasar. 31 Ba za a tuna da isashen abincin da aka samu a ƙasar ba,
domin yunwar da za tă biyo baya za tă zama da tsanani ƙwarai. 32 Dalilin da aka ba
wa Fir'auna mafarkan nan kashi biyu kuwa shi ne cewa Allah ya riga ya ƙaddara
al'amarin. Allah zai aikata shi, ba da daɗewa ba.

33 "Yanzu fa, bari Fir'auna yă nemi mutum mai basira da kuma hikima, yă sa shi
yă shugabanci ƙasar Masar. 34 Bari Fir'auna yă naɗa komishinoni a kan ƙasar don
su karɓi kashi ɗaya bisa biyar na girbin Masar a lokacin shekaru bakwai na yalwar
abinci. 35 Ya kamata su tara dukan abincin waɗannan shekaru masu kyau da suke
zuwa, su yi ajiyar hatsin a ƙarƙashin ikon Fir'auna, don a ajiye a birane don abinci.

36 Ya kamata a adana abincin nan don ƙasar, kāriya shekaru bakwai na yunwa, domin
a yi amfani da shi a lokacin shekarun yunwan da za su zo wa Masar, saboda kada
ƙasar ta lalace da yunwa."
37 Shirin ya yi wa Fir'auna da kuma dukan hafsoshinsa kyau. 38 Saboda haka
Fir'auna ya tambaye su, "Za mu iya samun wani kamar wannan mutum, wannan
wanda Ruhun Allah yake cikinsa?"*
39 Sai Fir'auna ya ce wa Yusuf, "Da yake Allah ya ba ka sanin dukan waɗannan,
babu wani mai basira da kuma hikima kamar ka. 40 Za ka shugabanci fadata, kuma
dukan mutanena za su zama a ƙarƙashinka. Da sarauta kaɗai zan fi ka girma."

*Yusuf shugaban Masar*

41 Saboda haka Fir'auna ya ce wa Yusuf, "Ga shi na sa ka zama shugaban dukan
ƙasar Masar." 42 Sa'an nan Fir'auna ya zare zoben sarauta daga yatsarsa, ya sa shi a
yatsan Yusuf. Ya sanya masa rigar lallausan lilin, ya kuma sa masa sarƙar zinariya a
wuyansa. 43 Ya sa shi ya hau keken yaƙi a matsayi mai binsa na biyu,† mutane kuwa
suka yi shela a gabansa suna cewa, "A ba da hanya!"‡ Ta haka ya sa shi shugaba a
kan dukan ƙasar Masar.
44 Sa'an nan Fir'auna ya ce wa Yusuf, "Ni ne Fir'auna, amma in ba tare da
umarninka ba, ba wanda zai ɗaga hannu ko ƙafa a cikin dukan Masar." 45 Fir'auna
ya ba wa Yusuf suna Zafenat-Faneya, ya kuma ba shi Asenat 'yar Fotifera firist na
On,§ ta zama matarsa. Yusuf kuwa ya zaga dukan ƙasar Masar.
46 Yusuf yana zuwa shekara talatin sa'ad da ya shiga hidimar Fir'auna sarkin Masar.
Yusuf kuwa ya fita daga gaban Fir'auna, ya zaga ko'ina a Masar. 47 A shekaru bakwai
na yalwa, ƙasar ta ba da amfani mai yawa. 48 Yusuf ya tattara dukan abincin da aka
samu a waɗannan shekaru bakwai na yalwa a Masar, ya kuma yi ajiyarsu a cikin
birane. A kowane birni, ya sa abincin da aka nome a kewayensa. 49 Sai Yusuf ya
tara hatsi da yawan gaske, kamar yashi a bakin teku, har sai da ya kāsa iya auna shi,
gama ba a iya aunawa.
50 Kafin shekarun yunwa su zo, Asenat 'yar Fotifera, firist na On, ta haifa wa Yusuf
'ya'ya maza biyu. 51 Yusuf ya ba wa ɗansa na fari suna Manasse* ya ce, "Gama Allah
ya sa na mance dukan wahalata da dukan gidan mahaifina." 52 Ya ba wa ɗansa na
biyu suna Efraim† ya ce, "Gama Allah ya wadata ni cikin wahalata."
53 Shekaru bakwai na yalwa a Masar suka zo ga ƙarshe, 54 sai shekaru bakwai na
yunwa suka soma shigowa, kamar yadda Yusuf ya faɗa. Aka yi yunwa ko'ina amma
ban da ƙasar Masar. Don akwai abinci. 55 Sa'ad da dukan Masar ta fara jin yunwa, sai
mutane suka yi wa Fir'auna kuka don abinci. Sai Fir'auna ya ce wa dukan Masarawa,
"Ku tafi wurin Yusuf, ku kuma yi abin da ya faɗa muku."
56 Sa'ad da yunwa ta bazu a dukan ƙasar, sai Yusuf ya buɗe gidajen ajiya, ya kuma
sayar da hatsi ga Masarawa, gama yunwa ta yi tsanani a dukan Masar. 57 Dukan
ƙasashe kuwa suka zo Masar don saya hatsi daga Yusuf, gama yunwa ta yi tsanani
a dukan duniya.

# 42

*'Yan'uwan Yusuf maza sun tafi Masar*

* **41:38** Ko kuwa na alloli † **41:43** Ko kuwa a cikin keken yaƙi ta muƙaddashinsa; ko kuwa cikin keken yaƙinsa ta biyu ‡ **41:43** Ko kuwa Rusuna § **41:45** Wato, Heliyofolis; haka ma a aya 50 * **41:51** Manasse ya yi kamar, kuma za a iya ɗauko daga kalmar Ibraniyanci mai ma'ana manta. † **41:52** Efraim ya yi kamar kalmar Ibraniyanci na wadata sau biyu.

1 Sa'ad da Yaƙub ya sami labari cewa akwai hatsi a Masar, sai ya ce wa 'ya'yansa
maza, "Don me kuke duban juna kawai?" 2 Ya ci gaba, "Na ji cewa akwai hatsi a
Masar. Ku gangara can ku sayo mana, domin mu rayu kada mu mutu."

3 Sai goma daga cikin 'yan'uwan Yusuf suka gangara don su saya hatsi daga Masar.
4 Amma Yaƙub bai aiki Benyamin, ɗan'uwan Yusuf tare da sauran ba, gama yana
tsoro kada wani abu yă faru da shi. 5 Sai 'ya'yan Yaƙub suka isa Masar tare da
sauran mutanen don sayen abinci, gama yunwar ta kai yankin Kan'ana ma.

6 To, Yusuf ne gwamnar ƙasar wanda yake sayar da hatsi ga dukan mutanenta.
Saboda haka sa'ad da 'yan'uwan Yusuf suka isa, sai suka rusuna masa har ƙasa da
fuskokinsu. 7 Nan da nan da Yusuf ya ga 'yan'uwansa, sai ya gane su, amma ya yi
kamar baƙo, ya kuma yi musu magana da tsawa. Ya tambaya, "Daga ina kuka fito?"

Suka amsa, "Daga ƙasar Kan'ana, don mu saya abinci."

8 Ko da yake Yusuf ya gane 'yan'uwansa, su ba su gane shi ba. 9 Sa'an nan ya tuna
da mafarkansa game da su, ya kuma ce musu, "Ku 'yan leƙen asiri ne! Kun zo don
ku leƙi asirin ƙasar ku ga inda ba ta da tsaro."

10 Suka amsa suka ce, "A'a, ranka yă daɗe, bayinka sun zo don saya abinci ne.
11 Mu duka 'ya'yan mutum ɗaya maza ne. Bayinka mutane ne masu gaskiya, ba 'yan
leƙen asiri ba ne."

12 Ya ce musu "Sam! Kun zo ne ku ga inda ƙasarmu babu tsaro."

13 Amma suka amsa suka ce, "Bayinka dā su goma sha biyu ne, 'yan'uwa, 'ya'yan
mutum guda maza, wanda yake zama a ƙasar Kan'ana. Karaminmu yanzu yana tare
da mahaifinmu, ɗayan kuma ya rasu."

14 Yusuf ya ce musu, "Daidai ne yadda na faɗa muku. Ku 'yan leƙen asiri ne! 15 Ga
kuwa yadda za a gwada ku. Muddin Fir'auna yana a raye, ba za ku bar wannan
wuri ba sai ƙaramin ɗan'uwanku ya zo nan. 16 Ku aiki ɗaya daga cikinku yă kawo
ɗan'uwanku; za a sa sauranku a kurkuku, saboda a gwada maganarku a ga ko gaskiya
ce kuke faɗi. In ba haka ba, to, da ran Fir'auna, ku 'yan leƙen asiri ne!" 17 Ya kuwa
sa su duka a kurkuku na kwana uku.

18 A rana ta uku, Yusuf ya ce musu, "Ku yi wannan za ku kuwa rayu, gama ina
tsoron Allah. 19 In ku mutane masu gaskiya ne, ku bar ɗaya daga cikin 'yan'uwanku
yă zauna a kurkuku, yayinda sauranku su tafi, su kai hatsi don gidajenku da suke
yunwa. 20 Amma dole ku kawo ƙaramin ɗan'uwanku gare ni, saboda a tabbatar da
maganarku har ba za ku mutu ba." Suka kuwa yi haka.

21 Sai suka ce wa juna, "Tabbatacce ana hukunta mu ne saboda ɗan'uwanmu. Mun
ga yadda ya yi wahala sa'ad da ya roƙe mu saboda ransa, amma ba mu saurare shi
ba, shi ya sa wannan wahala ta zo mana."

22 Ruben ya amsa, "Ban faɗa muku cewa kada ku ɗauki alhakin yaron nan ba, sai
kuka ƙi ji, to, yau ga alhakin jininsa muke biya." 23 Ba su san cewa Yusuf yana jin su
ba, da yake yana amfani da mai fassara ne.

24 Sai ya juya daga gare su ya yi kuka, sa'an nan ya dawo ya yi musu magana kuma.
Ya sa aka ɗauke Simeyon daga gare su, aka daure shi a idanunsu.

25 Yusuf ya yi umarni a cika buhunansu da hatsi, a kuma sa azurfan kowane mutum
a cikin buhunsa, a kuma ba su kalaci don tafiyarsu. Bayan aka yi musu wannan,
26 suka jibga hatsinsu a kan jakuna, sai suka kama hanya.

27 A wurin da suka tsaya don su kwana, ɗaya daga cikinsu ya buɗe buhunsa don yă
ciyar da jakinsa, sai ya ga azurfansa a bakin buhunsa. 28 Sai ya ce wa 'yan'uwansa,
"An mayar mini da azurfata. Ga shi a cikin buhuna."

Zuciyarsu ta karai, suka dubi juna suna rawan jiki, suka ce, "Mene ne wannan da
Allah ya yi mana?"

29 Sa'ad da suka zo wurin mahaifinsu Yaƙub a ƙasar Kan'ana, suka faɗa masa
dukan abin da ya faru da su. Suka ce, 30 "Mutumin da yake shugaba a ƙasar ya yi
mana matsananciyar magana, ya kuma ɗauke mu tamƙar 'yan leƙen asirin ƙasa.
31 Amma muka ce masa, 'Mu masu gaskiya ne; mu ba 'yan leƙen asiri ba ne. 32 Dā
mu 'yan'uwa ne goma sha biyu, 'ya'yan mahaifi guda maza. Ɗayanmu ya rasu, kuma
ƙaramin yanzu yana tare da mahaifinmu a Kan'ana.'

33 "Sai mutumin wanda yake shugaba a kan ƙasar ya ce mana, 'Ga yadda zan san
ko ku mutane masu gaskiya ne. Ku bar ɗaya daga cikin 'yan'uwanku a nan tare
da ni, ku ɗauki abinci domin gidajenku masu yunwa, ku tafi. 34 Amma ku kawo
mini ƙaramin ɗan'uwanku domin in san cewa ku ba 'yan leƙen asiri ba ne, amma
mutane ne masu gaskiya. Sa'an nan zan mayar muku da ɗan'uwanku, ku kuma iya
yin sana'a* a ƙasar.' "

35 Yayinda suke juyewa hatsi daga buhunansu, sai ga ƙunshin azurfan kowane
mutum a buhunsa! Sa'ad da su da mahaifinsu suka ga ƙunshe-ƙunshen kuɗi, suka
firgita. 36 Yaƙub mahaifinsu, ya ce musu, "Kun sa ni rashin 'ya'yana. Yusuf ya rasu,
Simeyon kuma ba ya nan, yanzu kuma kuna so ku ɗauki Benyamin. Kome yana gāba
da ni!"

37 Sai Ruben ya ce wa mahaifinsa, "Ka kashe dukan 'ya'yana maza, in ban dawo
da shi gare ka ba. Ka sa shi ga kulawata, zan kuwa dawo da shi."

38 Amma Yaƙub ya ce, "Ɗana ba zai gangara zuwa can tare da ku ba, ɗan'uwansa
ya rasu, shi ne kaɗai ya rage. In wani abu ya faru da shi a tafiyar da za ku yi, za ku
sa furfurata ta gangara zuwa kabari† cikin baƙin ciki."

# 43

*Tafiya ta biyu zuwa Masar*

1 A yanzu, yunwa ta yi tsanani a ƙasar. 2 Saboda haka sa'ad da suka cinye dukan
hatsin da suka kawo daga Masar, mahaifinsu ya ce musu, "Ku koma, ku sayo mana
ƙarin abinci."

3 Amma Yahuda ya ce masa, "Mutumin ya gargaɗe mu sosai cewa, 'Ba za ku sāke
ganin fuskata ba sai in ɗan'uwanku yana tare da ku.' 4 In za ka aika da ɗan'uwanmu
tare da mu, za mu gangara mu sayo maka abinci. 5 Amma in ba za ka aika da shi ba,
ba za mu gangara ba, gama mutumin ya ce mana, 'Ba za ku sāke ganin fuskata ba
sai ko in ɗan'uwanku yana tare da ku.' "

6 Isra'ila ya yi tambaya, "Me ya sa kuka kawo wannan damuwa a kaina ta wurin
faɗa wa mutumin cewa kuna da wani ɗan'uwa?"

7 Suka amsa, "Mutumin ya yi mana tambaya sosai game da kanmu da iyalinmu.
Ya tambaye mu, 'Mahaifinku yana da rai har yanzu? Kuna da wani ɗan'uwa?' Mu
dai mun amsa tambayoyinsa ne. Ta yaya za mu sani zai ce, 'Ku kawo ɗan'uwanku a
nan'?"

8 Sa'an nan Yahuda ya ce wa Isra'ila mahaifinsa, "Ka aika saurayin tare da ni za mu
kuwa tafi nan da nan, saboda mu da 'ya'yanmu mu rayu, kada mu mutu. 9 Ni kaina
zan tabbatar da lafiyarsa; na ɗauki lamuninsa, a hannuna za ka neme shi. In ban
dawo da shi gare ka, in sa shi nan a gabanka ba, zan ɗauki laifin a gabanka dukan
kwanakina. 10 Ai, da ba mun jinkirta ba, da mun komo har sau biyu."

11 Sa'an nan mahaifinsu Isra'ila ya ce musu, "In dole ne a yi haka, to, sai ku yi.
Ku sa waɗansu amfani mafi kyau na ƙasar a buhunanku, ku ɗauka zuwa wurin
mutumin a matsayin kyauta, da ɗan man ƙanshi na shafawa, da kuma 'yar zuma,
da kayan yaji, da ƙaro, da tsabar citta da kuma almon. 12 Ku ɗauki ninki biyu na
yawan azurfa tare da ku, gama dole ku mayar da azurfan da aka sa a cikin bakunan

* 42:34 Ko kuwa ma'amala a sake † 42:38 Da Ibraniyanci Sheol.

buhunanku. Mai yiwuwa an yi haka a kuskure ne. 13 Ku ɗauki ɗan'uwanku kuma
ku koma wurin mutumin nan da nan. 14 Bari Allah Maɗaukaki* yă nuna muku alheri
a gaban mutumin saboda yă bar ɗan'uwanku da Benyamin su dawo tare da ku. Ni
kuwa, in na yi rashi, na yi rashi."
15 Saboda haka mutanen suka ɗauki kyautar, da kuma kuɗin da ya ninka na farko.
Suka kuma ɗauki Benyamin, suka gaggauta suka gangara zuwa Masar suka kuma
gabatar da kansu ga Yusuf. 16 Sa'ad da Yusuf ya ga Benyamin tare da su, sai ya ce wa
mai hidimar gidansa, "Ka shigar da mutanen cikin gida, ka yanka dabba ka shirya,
gama mutanen za su ci abincin rana tare da ni."
17 Mutumin ya yi kamar yadda Yusuf ya faɗa masa, ya kuwa ɗauki mutanen zuwa
gidan Yusuf. 18 Mutanen dai suka firgita sa'ad da aka ɗauke su zuwa gidansa. Suka
yi tunani, "An kawo mu nan ne saboda azurfan da aka sa a cikin buhunanmu da
farko. Yana so yă fāɗa mana, yă kuma sha ƙarfinmu, yă ƙwace mu kamar bayi, yă
kuma kwashe jakunanmu."
19 Saboda haka suka je wurin mai yin wa Yusuf hidima, suka yi masa magana a
bakin ƙofar gida. 20 Suka ce, "Ranka yă daɗe, mun zo nan ƙaro na farko don mu
saya abinci, 21 amma a inda muka tsaya don mu kwana, da muka buɗe buhunanmu
sai kowannenmu ya sami azurfansa daidai a bakin buhunsa. Saboda haka ga kuɗin
a hannunmu, mun sāke komowa da su. 22 Mun kuma kawo ƙarin azurfa tare da mu
don mu saya abinci. Ba mu san wa ya sa azurfanmu a cikin buhunanmu ba."
23 Sai mai hidimar ya ce, "Ba kome, kada ku ji tsoro. Allahnku, Allahn mahaifinku
ne ya ba ku dukiyar a cikin buhunanku; ni dai, na karɓi azurfanku." Sa'an nan ya
fitar musu da Simeyon.
24 Mai yin hidimar ya ɗauki mutane zuwa gidan Yusuf ya ba su ruwa su wanke
ƙafafunsu, ya kuma tanada wa jakunansu abinci. 25 Suka shirya kyautansu domin
isowar Yusuf da rana, gama sun ji cewa zai ci abinci a nan.
26 Sa'ad da Yusuf ya zo gida, sai suka ba shi kyautai da suka kawo, suka rusuna a
gabansa har ƙasa. 27 Ya tambaye su, yaya suke, sa'an nan ya ce, "Yaya tsohon nan
mahaifinku da kuka faɗa mini? Yana da rai har yanzu?"
28 Suka amsa, "Bawanka mahaifinmu yana da rai har yanzu da kuma ƙoshin lafiya."
Suka kuma rusuna suka yi mubaya'a.
29 Da ya ɗaga idanu, sai ya ga ɗan'uwansa Benyamin, ɗan mahaifiyarsa, sai ya
yi tambaya, "Wannan ne ƙaramin ɗan'uwanku, wanda kuka faɗa mini a kai?" Ya
kuma ce, "Allah yă yi maka albarka, ɗana." 30 Saboda motsi mai zurfi da zuciyarsa
ta yi da ganin ɗan'uwansa, sai Yusuf ya gaggauta ya fita, ya nemi wuri yă yi kuka.
Ya shiga ɗakinsa ya yi kuka a can.
31 Bayan ya wanke fuskarsa, sai ya fito ya daure, ya umarta, "A kawo abinci."
32 Sai aka raba musu abinci, nasa shi kaɗai su kuma su kaɗai, domin Masarawa ba
sa cin abinci tare da Ibraniyawa, gama wannan abin ƙyama ne ga Masarawa. 33 Aka
zaunar da 'yan'uwan Yusuf a gabansa bisa ga shekarunsu, daga ɗan fari zuwa auta.
'Yan'uwan kuwa suka duddubi juna suna mamaki. 34 Daga teburin da yake a gaban
Yusuf aka riƙa ɗibar rabonsu ana kai musu, amma rabon Benyamin ya yi biyar ɗin
na kowannensu. Suka kuwa sha, suka yi murna tare da shi.

# 44

*Kwaf Azurfa a cikin buhu*

1 Yusuf kuwa ya ba wa mai yin masa hidima a gida, waɗannan umarnai cewa,
"Cika buhunan mutanen nan da abinci iyakar yadda za su iya ɗauka, ka kuma sa

* **43:14** Da Ibraniyanci an rubuta El-Shaddai ne.

kuɗin kowanne a bakin buhunsa. 2 Sa'an nan ka sa kwaf nawa, wannan na azurfa
a bakin buhun autan, tare da kuɗinsa na hatsi.” Sai mai hidimar ya yi kamar yadda
Yusuf ya umarta.
3 Da gari ya waye, sai aka sallami mutanen tare da jakunansu. 4 Ba su yi nisa da
birnin ba sa'ad da Yusuf ya ce wa mai yin masa hidima, “Tashi, ka bi waɗannan
mutane nan da nan, in ka same su, ka ce musu, ‘Me ya sa kuka sāka alheri da
mugunta? 5 Ba da wannan kwaf ne maigidana yake sha daga ciki yana kuma yin
amfani da shi don duba? Wannan mugun abu ne da kuka yi.’ ”
6 Sa'ad da ya same su, sai ya maimaita waɗannan kalmomi gare su. 7 Amma suka
ce masa, “Me ya sa ranka yǎ daɗe yake faɗin irin waɗannan abubuwa? Allah yǎ
sawwaƙe bayinka su yi irin wannan abu! 8 Mun ma dawo maka da kuɗin da muka
samu a cikin bakunan buhunanmu daga ƙasar Kan'ana. Saboda haka me zai sa mu
saci azurfa ko zinariya daga gidan maigidanka? 9 In aka sami wani daga cikin bayinka
da shi, zai mutu; sai sauran su zama bayin mai girma.”
10 Sai ya ce, “To, shi ke nan, bari yǎ zama yadda kuka faɗa. Duk wanda aka same
shi da kwaf na azurfan zai zama bawana, sauran kuwa za su 'yantu daga zargin.”
11 Da sauri kowannensu ya sauko da buhunsa ƙasa, ya buɗe. 12 Sa'an nan mai
hidimar ya fara bincike, farawa daga babba, ya ƙare a ƙaramin. Aka kuwa sami
kwaf ɗin a buhun Benyamin. 13 Ganin wannan sai suka kyakkece rigunansu. Sa'an
nan suka jibga wa jakunansu kaya, suka koma birni.
14 Yusuf yana nan har yanzu a gida sa'ad da Yahuda da 'yan'uwansa suka shiga,
suka fāɗi rub da ciki a ƙasa a gabansa. 15 Yusuf ya ce musu, “Mene ne wannan da
kuka yi? Ba ku san cewa mutum kamar ni yana iya gane abubuwa ta wurin duba
ba?”
16 Yahuda ya amsa ya ce, “Me za mu ce wa ranka yǎ daɗe? Yaya kuma za mu
wanke kanmu daga wannan zargi? Allah ya tona laifin bayinka. Ga mu, za mu zama
bayinka, da mu da wanda aka sami kwaf ɗin a hannunsa.”
17 Amma Yusuf ya ce, “Allah yǎ sawwaƙe in yi haka! Mutumin da aka sami kwaf
ɗin a hannunsa ne kaɗai zai zama bawana. Sauranku, ku koma ga mahaifinku da
salama.”
18 Sai Yahuda ya haura zuwa wurinsa ya ce, “Ranka yǎ daɗe, roƙo nake, bari
bawanka yǎ yi magana da ranka yǎ daɗe. Kada ka yi fushi da bawanka, ko da yake
daidai kake da Fir'auna kansa. 19 Ranka yǎ daɗe ya tambayi bayinka ya ce, ‘Kuna da
mahaifi ko ɗan'uwa?’ 20 Muka kuwa amsa, ‘Muna da mahaifi tsoho, akwai kuma ɗa
matashi, wanda aka haifa masa cikin tsufarsa. Ɗan'uwansa ya rasu, shi ne kuwa ɗa
kaɗai na mahaifiyarsa da ya rage, mahaifinsa kuwa yana ƙaunarsa.’
21 “Sai ka ce wa bayinka, ‘Ku kawo mini shi don in gan shi da kaina.’ 22 Muka
kuwa ce wa ranka yǎ daɗe, ‘Saurayin ba zai iya barin mahaifinsa ba, gama in ya
bar shi, mahaifinsa zai mutu.’ 23 Amma ka faɗa wa bayinka, ‘Sai kun kawo ƙaramin
ɗan'uwanku tare da ku, in ba haka ba, ba za ku sāke ganin fuskata ba.’ 24 Sa'ad da
muka koma wurin bawanka mahaifinmu, sai muka faɗa masa abin da ranka yǎ daɗe
ya ce.
25 “Sai mahaifinmu ya ce, ‘Ku koma ku sayo ƙarin abinci.’ 26 Amma muka ce, ‘Ba
za mu iya gangarawa ba, sai in ƙaramin ɗan'uwanmu yana tare da mu. Ba za mu
iya ganin fuskar mutumin ba, sai ƙaramin ɗan'uwanmu yana tare mu.’
27 “Bawanka mahaifinmu ya ce mana, ‘Kun san cewa matata ta haifa mini 'ya'ya
biyu maza. 28 Dayansu ya tafi daga gare ni, na kuwa ce, “Tabbatacce an yayyage shi
kaca-kaca.” Ban kuwa gan shi ba tuntuni. 29 In kun ɗauki wannan daga wurina shi
ma wani abu ya same shi, za ku kawo furfura kaina zuwa kabari* cikin baƙin ciki.’

* **44:29** Da Ibraniyanci Sheol; haka kuma a aya 31.

30 “Saboda haka yanzu, in saurayin ba ya nan tare da mu sa’ad da na koma ga
bawanka mahaifina, in kuma mahaifina, wanda ransa yana daure kurkusa da ran
saurayin, 31 ya ga cewa saurayin ba ya nan, zai mutu. Bayinka za su sa bawanka,
mahaifinmu, yǎ mutu cikin baƙin ciki, da tsufansa. 32 Gama ni baranka na ɗauki
lamunin saurayin a wurin mahaifinsa da cewa, ‘In ban komo maka da shi ba, sai
alhakinsa yǎ zauna a kaina a gaban mahaifina, dukan raina!’

33 “To, yanzu, ina roƙonka bari bawanka yǎ zauna a nan a matsayin bawanka,
ranka yǎ daɗe a maimakon saurayin, a kuma bar saurayin yǎ koma da ’yan’uwansa.
34 Yaya zan koma ga mahaifina, in saurayin ba ya tare da ni? A’a! Kada ka bari in ga
baƙin cikin da zai auko wa mahaifina.”

# 45

### *Yusuf ya sanar da kansa*

1 Yusuf bai ƙara iya daurewa a gaban dukan masu yi masa hidima ba, sai ya yi kuka
da ƙarfi ya ce, “Kowa yǎ tashi daga gabana!” Saboda haka ba kowa a wurin sa’ad
da Yusuf ya sanar da kansa ga ’yan’uwansa. 2 Sai ya yi kuka da ƙarfi har Masarawa
suka ji, har labarin ya kai gidan Fir’auna.

3 Yusuf kuwa ya ce wa ’yan’uwansa, “Ni ne Yusuf! Mahaifina yana nan da rai har
yanzu?” Amma ’yan’uwansa ba su iya amsa masa ba, gama sun firgita ƙwarai a
gabansa.

4 Sa’an nan Yusuf ya ce wa ’yan’uwansa, “Ku zo kusa da ni.” Da suka yi haka, sai
ya ce, “Ni ne ɗan’uwanku Yusuf, wannan da kuka sayar zuwa Masar! 5 Yanzu dai,
kada ku damu, kada kuma ku yi fushi da kanku saboda kun sayar da ni a nan, gama
Allah ya aiko ni gabanku ne don in ceci rayuka. 6 Ga shi shekaru biyu ke nan ake
yunwa a ƙasar, kuma da sauran shekara biyar masu zuwa da ba za a yi noma ko
girbi ba. 7 Amma Allah ya aiko ni gabanku ne don in adana muku raguwa a duniya,
in kuma ceci rayukanku ta wurin ceto* mai girma.

8 “Saboda haka fa, ba ku ba ne kuka aiko ni nan, Allah ne. Ya mai da ni mahaifi
ga Fir’auna, shugaban dukan gidansa da kuma mai mulkin dukan Masar. 9 Yanzu sai
ku gaggauta zuwa wurin mahaifina ku faɗa masa, ‘Abin da ɗanka Yusuf ya ce; Allah
ya mai da ni shugaban dukan Masar. Gangaro wurina; kada ka jinkirta. 10 Za ka yi
zama a yankin Goshen, ka kasance kusa da ni. Kai, ’ya’yanka da kuma jikokinka,
garkunanka da shanunka, da kuma dukan abin da kake da shi. 11 Zan tanada maka
a nan, domin akwai saura shekaru biyar na yunwa masu zuwa. In ba haka ba, kai
da gidanka da dukan mallakarka za ku zama gajiyayyu.’

12 “Ku kanku kun gani, haka ma ɗan’uwana Benyamin, cewa tabbatacce ni ne nake
magana da ku. 13 Faɗa wa mahaifina game da dukan girman da aka ba ni a Masar,
da kuma game da kome da kuka gani. Ku kuma kawo mahaifina a nan da sauri.”

14 Sa’an nan ya rungume ɗan’uwansa Benyamin ya yi kuka, sai Benyamin ya
rungume shi yana kuka. 15 Ya sumbaci dukan ’yan’uwansa, ya kuma yi kuka a kansu.
Bayan haka sai ’yan’uwansa suka yi masa magana.

16 Sa’ad da labarin ya kai fadan Fir’auna cewa ’yan’uwan Yusuf sun zo, sai
Fir’auna da dukan hafsoshin suka ji daɗi. 17 Fir’auna ya ce wa Yusuf, “Faɗa wa
’yan’uwanka, ‘Yi wannan; ku jibge dabbobinku ku koma zuwa ƙasar Kan’ana, 18 Ku
kawo mahaifinku da iyalanku zuwa wurina. Zan ba ku mafi kyau na ƙasar Masar,
za ku kuwa ci moriyar ƙasar.’

* **45:7** Ko kuwa cece ka kamar ƙungiya mai girma da suka tsira

19 “An kuma umarce ka, ka faɗa musu, ‘Ku yi wannan, ku ɗauki wagonu daga
Masar domin ’ya’yanku da matanku, ku ɗauki mahaifinku ku zo. 20 Kada ku damu
da mallakarku, gama mafi kyau na Masar za su zama naku.’ ”

21 Sai ’ya’yan Isra’ila maza suka yi haka. Yusuf ya ba su wagonu kamar yadda
Fir’auna ya umarta, ya kuma ba su guzuri don tafiyarsu. 22 Ya ba da sababbin riguna
ga kowannensu amma ga Benyamin ya ba shi shekel† ɗari uku na azurfa da riguna
kashi biyar. 23 Ga kuma abin da ya aika wa mahaifinsa, jakuna goma da aka jibge da
abubuwa mafi kyau na Masar, da jakuna mata guda goma ɗauke da hatsi da burodi da
waɗansu tanade-tanade don tafiyarsa. 24 Sa’an nan ya sallami ’yan’uwansa, yayinda
suke barin wurin ya ce musu, “Kada ku yi faɗa a hanya!”

25 Saboda haka suka haura, suka fita daga Masar, suka zo wurin maihaifinsu Yaƙub
a ƙasar Kan’ana. 26 Suka faɗa masa, “Yusuf yana da rai! Gaskiya, shi ne mai mulkin
dukan Masar.” Gaban Yaƙub ya fāɗi, domin bai gaskata su ba. 27 Amma sa’ad da suka
faɗa masa kome da Yusuf ya faɗa musu, da kuma sa’ad da ya ga wagonun da Yusuf
ya aika don a ɗauke shi a kai da shi can, sai ya farfaɗo, ya dawo cikin hankalinsa.
28 Sai Yaƙub ya ce, “Na yarda! Ɗana Yusuf yana da rai har yanzu. Zan tafi in gan shi
kafin in mutu.”

# 46

*Yaƙub ya tafi Masar*

1 Saboda haka Isra’ila ya kama hanya da dukan abin da yake nasa, sa’ad da ya kai
Beyersheba, sai ya miƙa hadayu ga Allah na Ishaku, mahaifinsa.

2 Allah kuwa ya yi magana ga Isra’ila a wahayi da dare ya ce, “Yaƙub! Yaƙub!”

Yaƙub kuwa ya amsa ya ce, “Ga ni.”

3 Sai Allah ya ce, “Ni ne Allah, Allah na mahaifinka. Kada ka ji tsoron zuwa Masar,
gama zan mai da kai al’umma mai girma a can. 4 Zan gangara zuwa Masar tare da
kai, tabbatacce zan sāke dawo da kai. Kuma hannun Yusuf zai rufe idanunka.”

5 Sa’an nan Yaƙub ya bar Beyersheba, ’ya’yan Isra’ila maza, suka ɗauki mahaifinsu
Yaƙub da ’ya’yansu da matansu a cikin wagonun da Fir’auna ya aika don a kawo
shi. 6 Suka kuma ɗauki dabbobinsu da mallakarsu, da suka samu a Kan’ana, Yaƙub
kuwa da dukan zuriyarsa suka tafi Masar. 7 Ya ɗauki ’ya’yansa maza da jikokinsa da
’ya’yansa mata da jikokinsa mata, dukan zuriyarsa zuwa Masar.

8 Waɗannan su ne sunayen ’ya’yan Isra’ila maza (Yaƙub da zuriyarsa)
waɗanda suka tafi Masar,

Ruben ɗan farin Yaƙub.
9 ’Ya’yan Ruben maza su ne,
Hanok, Fallu, Hezron da Karmi.
10 ’Ya’yan Simeyon maza su ne,
Yemuwel, Yamin, Ohad, Yakin, Zohar da Sha’ul ɗan mutuniyar Kan’ana.
11 ’Ya’yan Lawi maza su ne,
Gershon, Kohat da Merari.
12 ’Ya’yan Yahuda maza su ne,
Er, Onan, Shela, Ferez da Zera (amma Er da Onan sun mutu a ƙasar Kan’ana).
’Ya’yan Ferez maza su ne,
Hezron da Hamul.
13 ’Ya’yan Issakar maza su ne,

† **45:22** Wato, kamar fam bakwai da rabi (kamar kilo 3.5)

Tola, Fuwa,* Yoshub† da Shimron.
14 ’Ya’yan Zebulun maza su ne,
Sered, Elon da Yaleyel.
15 Waɗannan su ne ’ya’yan Liyatu maza da ta haifa wa Yaƙub a Faddan Aram,‡ ban da ’yarsa Dina. ’Ya’yansa maza da mata duka, mutum talatin da uku ne.

16 ’Ya’yan Gad maza su ne,
Zafon,§ Haggi, Shuni, Ezbon, Eri, Arodi da Areli.
17 ’Ya’yan Asher maza su ne,
Imna, Ishba, Ishbi da Beriya. ’Yar’uwarsu ita ce Sera.
’Ya’yan Beriya maza su ne,
Heber da Malkiyel.
18 Waɗannan su ne ’ya’yan da Zilfa ta haifa wa Yaƙub, ita ce Laban ya ba wa ’yarsa Liyatu. ’Ya’yan duka, su sha shida ne.

19 ’Ya’yan Yaƙub maza waɗanda Rahila ta haifa su ne,
Yusuf da Benyamin.
20 A Masar, Asenat ’yar Fotifera, firist na On* ta haifi Manasse da Efraim wa Yusuf.
21 ’Ya’yan Benyamin maza su ne,
Bela, Beker, Ashbel, Gera, Na’aman, Ehi, Rosh, Muffim, Huffim da Ard.
22 Waɗannan su ne ’ya’yan Rahila maza waɗanda ta haifa wa Yaƙub, dukansu mutum goma sha huɗu ne.

23 Yaron Dan shi ne,
Hushim.
24 ’Ya’yan Naftali maza su ne,
Yazeyel, Guni, Yezer da Shillem.
25 Waɗannan su ne ’ya’ya mazan da Bilha ta haifa wa Yaƙub, ita ce Laban ya ba wa ’yarsa Rahila. ’Ya’yan suka su bakwai ne.

26 Dukan waɗanda suka tafi Masar tare da Yaƙub, waɗanda suke zuriyarsa
kai tsaye ban da matan ’ya’yansa maza, su mutum sittin da shida ne. 27 In
aka haɗa da ’ya’yan nan maza† guda biyu waɗanda aka haifa wa Yusuf a Masar, membobin iyalin Yaƙub, waɗanda suka tafi Masar, duka su saba’in‡ ne.

28 To, Yaƙub ya aiki Yahuda yă yi gaba yă sadu da Yusuf, don yă nuna musu hanyar
da za su bi zuwa yankin Goshen. Da suka isa yankin Goshen, 29 sai Yusuf ya kintsa
keken yaƙinsa ya haura zuwa Goshen don yă taryi mahaifinsa, Isra’ila. Nan da nan da isowar Yusuf a wurin mahaifinsa, sai ya rungumi mahaifinsa§, ya yi kuka na dogon lokaci.
30 Isra’ila ya ce wa Yusuf, “Yanzu ina a shirye in mutu, da yake na gani da kaina cewa har yanzu kana da rai.”

* **46:13** Fentatut na Samariya da na Assuriya (dubi kuma 1Tar 7.1); Rubuce-rubucen Masoretik na da Fuwa ne.
† **46:13** Fentatut na Samariya da waɗansu Seftuwajin (dubi Kid 26.24 da 1Tar 7.1); rubuce-rubucen Masoretik.
‡ **46:15** Wato, arewa maso yamman Mesofotamiya § **46:16** Fentatut Samariya da Seftuwajin (dubi kuma Kid 26.15); rubuce-rubucen Masoretik Zifiyon. * **46:20** Wato, Heliyofolis † **46:27** Da Ibraniyanci; Seftuwajin, yara tara ‡ **46:27** Da Ibraniyanci (dubi kuma Fit 1.5 da kuma fassara ƙasar shafi); Seftuwajin (dubi kuma Ayy M 7.14) saba’in da biyar. § **46:29** Da Ibraniyanci kewaye da shi.

31 Sa'an nan Yusuf ya ce wa 'yan'uwansa da gidan mahaifinsa, "Zan haura in yi
magana da Fir'auna, zan kuwa ce masa, ''Yan'uwana da gidan mahaifina, waɗanda
suke zaune a ƙasar Kan'ana, sun zo wurina. 32 Mutanen fa, makiyaya ne; suna
kiwon dabbobi, sun kuma zo tare da garkunansu da shanunsa da kuma kome da suka
mallaka.' 33 Sa'ad da Fir'auna ya kira ku ciki, ya yi tambaya, 'Mece ce sana'arku?'
34 Ku amsa, 'Bayinka suna kiwon dabbobi ne, tun muna samari har zuwa yanzu,
kamar yadda kakanninmu suka yi.' Ta haka za a bar ku ku zauna a yankin Goshen,
gama Masarawa suna ƙyamar makiyaya."

# 47

1 Yusuf ya tafi yă faɗa wa Fir'auna, "Mahaifina da 'yan'uwana, tare da garkunansu
da shanunsu da kome da suke da shi, sun zo daga ƙasar Kan'ana, suna kuwa a Goshen
yanzu."
2 Sai ya zaɓi mutum biyar daga cikin 'yan'uwansa, ya gabatar da su a gaban
Fir'auna.
3 Fir'auna ya tambayi 'yan'uwan, "Mece ce sana'arku?"
Suka amsa wa Fir'auna suka ce, "Bayinka makiyaya ne, kamar yadda kakanninmu
suke." 4 Suka kuma ce masa, "Mun zo, mu zauna a nan na ɗan lokaci, gama yunwa
ta yi tsanani a Kan'ana, dabbobin bayinka kuma ba su da wurin kiwo. Saboda haka
yanzu, muna roƙonka, bari bayinka su zauna a Goshen."
5 Fir'auna ya ce wa Yusuf, "Mahaifinka da 'yan'uwanka sun zo maka, 6 ƙasar Masar
kuma tana gabanka, ka zaunar da mahaifinka da 'yan'uwanka a sashe mafi kyau na
ƙasar, bari su zauna a Goshen. Idan kuma ka ga waɗansu a cikinsu da suka fi dacewa,
sai ka sa su lura mini da shanuna."
7 Sa'an nan Yusuf ya shigar da Yaƙub mahaifinsa, ya gabatar da shi a gaban
Fir'auna. Bayan Yaƙub ya albarkaci* Fir'auna, 8 sai Fir'auna ya tambaye shi,
"Shekarunka nawa da haihuwa?"
9 Yaƙub kuwa ya ce wa Fir'auna, "Shekarun hijirata, shekaru ɗari da talatin ne.
Shekaruna kaɗan ne cike da wahala, ba za a kuwa daidaita su da shekarun hijirar
kakannina ba." 10 Sai Yaƙub ya albarkaci† Fir'auna, ya yi masa bankwana, sa'an nan
ya fita.
11 Ta haka Yusuf ya zaunar da mahaifinsa da 'yan'uwansa a Masar, ya ba su mallaka
a sashe mafi kyau na ƙasar, a yankin nan na Rameses, kamar yadda Fir'auna ya
umarta. 12 Yusuf ya kuma tanada wa mahaifinsa da kuma 'yan'uwansa da dukan
gidan mahaifinsa, abinci bisa ga yawan 'ya'yansu.

### *Hidimar Yusuf a lokacin yunwa*

13 A yanzu, a cikin ƙasar duka, ba abinci, gama yunwa ta yi tsanani ƙwarai, har
ƙasar Masar da ƙasar Kan'ana suka shiga matsanancin wahala! 14 Yusuf ya tattara
dukan kuɗaɗen da suke a Masar da Kan'ana don biyan hatsin da suke saya, ya kuwa
kawo su a fadan Fir'auna. 15 Sa'ad da kuɗin mutanen Masar da Kan'ana suka ƙare,
dukan Masar ta zo wurin Yusuf ta ce, "Ka ba mu abinci. Me zai sa mu mutu a
idanunka? Kuɗinmu duk sun ƙare."
16 Yusuf ya ce, "To, ku kawo dabbobinku, zan sayar muku da abinci a madadin
dabbobinku, tun da kuɗinku ya ƙare." 17 Saboda haka suka kawo dabbobinsu
wa Yusuf, ya kuma ba su abinci a madadin dawakai, tumaki da awaki, shanu da
jakunansu. Ya kuwa ba su abinci a madadin dabbobinsu, a wannan shekara.
18 Sa'ad da wannan shekara ta ƙare, sai suka zo wurinsa a shekara ta biye suka
ce, "Ba za mu ɓoye maka ba ranka yă daɗe, kuɗinmu sun ƙare, dabbobinmu kuma
sun zama naka. Ranka yă daɗe, in ban da jikunanmu da gonakinmu, ba abin da ya

* **47:7** Ko kuwa gai da † **47:10** Ko kuwa ya yi bankwana da

rage mana. 19 Kada ka bar mu mu mutu, ka yi wata dabara! Kada ka bari mu rasa
gonakinmu. Ka musaye mu da abinci, mu da gonakinmu. Mu kuwa za mu zama
bayin Fir'auna. Ka ba mu iri don mu rayu, kada mu mutu, don kuma kada gonakin
ƙasarmu su zama kango."
20 Ta haka Yusuf ya saya wa Fir'auna ƙasar Masar duka, gama Masarawa duka
sun sayar da gonakinsu, saboda yunwa ta tsananta musu. Kasar ta zama mallakar
Fir'auna. 21 Yusuf kuwa ya mai da mutanen bayi‡, daga wannan iyakar Masar zuwa
wancan. 22 Amma bai sayi gonakin firistoci ba, gama suna karɓa rabo daga Fir'auna
ne, suna kuma da isashen abinci daga rabon da Fir'auna yake ba su. Dalilin ke nan
da ba su sayar da gonakinsu ba.
23 Yusuf ya ce wa mutane, "Yanzu da na saye ku da kuma gonakinku a yau wa
Fir'auna, ga iri don ku shuka a gonaki. 24 Amma sa'ad da hatsi suka nuna, za ku ba
da kashi ɗaya bisa biyar ga Fir'auna. Sauran kashi huɗu bisa biyar kuma ku riƙe a
matsayin iri don gonaki da kuma abinci wa kanku da gidajenku da kuma 'ya'yanku."
25 Suka ce, "Ka ceci rayukanmu, in ya gamshe ka, ranka yǎ daɗe, za mu zama bayin
Fir'auna."
26 Ta haka Yusuf ya kafa wannan ya zama doka game da ƙasa a Masar, har yǎ
zuwa yau cewa kashi ɗaya bisa biyar na amfani gona ya zama na Fir'auna. Gonakin
firistoci ne kaɗai ba su zama na Fir'auna ba.
27 To, Isra'ilawa suka zauna a Masar a yankin Goshen. Suka mallaki filaye a can,
suka riɓaɓɓanya suka ƙaru ƙwarai.
28 Yaƙub ya yi zama a Masar shekaru goma sha bakwai, yawan shekarunsa duka
sun zama ɗari da arba'in da bakwai. 29 Sa'ad da lokaci ya gabato da Isra'ila zai mutu,
sai ya kira ɗansa Yusuf, ya ce masa, "Ka yi mini wannan alheri, ka sa hannunka
ƙarƙashin cinyar ƙafata, ka yi mini alkawari saboda ina roƙonka kaɗa ka bizne ni a
Masar, 30 amma sa'ad da na huta da kakannina, ka ɗauke ni, ka fid da ni daga Masar,
ka binne ni a inda aka binne su."
Yusuf ya ce, "Zan yi yadda ka faɗa."
31 Yaƙub ya ce, "Ka rantse mini." Sai Yusuf ya rantse masa, Isra'ila kuwa ya yi
godiya ga Allah yayinda ya jingina a kan sandansa.§

# 48

*Manasse da Efraim*

1 Bayan wani lokaci aka faɗa wa Yusuf, "Mahaifinka yana ciwo." Sai ya ɗauki
'ya'yansa maza biyu, Manasse da Efraim suka tafi tare da shi. 2 Sa'ad da aka faɗa wa
Yaƙub, "Ɗanka Yusuf ya zo gare ka," sai Isra'ila ya ƙoƙarta ya tashi ya zauna a kan
gado.
3 Yaƙub ya ce wa Yusuf, "Allah Maɗaukaki* ya bayyana gare ni a Luz a ƙasar
Kan'ana, a can ya albarkace ni 4 ya kuma ce mini, 'Zan sa ka yi ta haihuwa ka kuma
riɓaɓɓanya, za ka ƙaru a yawa. Zan mai da kai al'ummar mutane, zan kuma ba ka
wannan ƙasa tǎ zama madawwamiyar mallaka ga zuriyarka a bayanka.'
5 "To, yanzu, 'ya'ya mazanka biyu da aka haifa maka a Masar kafin in zo a nan
za su zama nawa; Efraim da Manasse za su zama nawa, kamar yadda Ruben da
Simeyon suke nawa. 6 Duk waɗansu 'ya'yan da aka haifa maka bayansu za su zama
naka; a yankin da suka gāda za a lissafa a ƙarƙashin sunayen 'yan'uwansu. 7 Yayinda
nake dawowa daga Faddan Aram,† cikin baƙin cikina Rahila ta rasu a ƙasar Kan'ana

‡ **47:21** Fentatut da Seftuwajin (dubi kuma Bulget); Masoretik ya kai mutane zuwa birane. § **47:31** Ko kuwa Isra'ila ya rusuna a kan gadonsa * **48:3** Da Ibraniyanci El-Shaddai † **48:7** Wato, arewa maso yamman Mesofotamiya

yayinda muke kan hanya, ʼyar rata daga Efrata. Saboda haka na binne ta a can kusa da hanya zuwa Efrata” (wato, Betlehem).

8 Saʼad da Israʼila ya ga ʼyaʼyan Yusuf maza, sai ya yi tambaya, “Su wane ne waɗannan?”

9 Yusuf ya ce wa mahaifinsa, “Su ne ʼyaʼyan da Allah ya ba ni a nan.”

Saʼan nan Israʼila ya ce, “Kawo mini su saboda in albarkace su.”

10 Yanzu fa idanun Israʼila sun fara rasa ƙarfi saboda tsufa, har ba ya iya gani sosai. Saboda haka Yusuf ya kawo ʼyaʼyansa maza kusa da shi, sai mahaifinsa ya sumbace su ya rungume su.

11 Israʼila ya ce wa Yusuf, “Ban yi tsammani zan ga fuskarka kuma ba, yanzu kuwa Allah ya bar ni in ga ʼyaʼyanka su ma.”

12 Saʼan nan Yusuf ya ɗauke su daga gwiwoyin Israʼila ya rusuna da fuskarsa har
ƙasa. 13 Yusuf ya ɗauke su biyu, Efraim a damansa zuwa hagun Israʼila, Manasse
kuma a hagunsa zuwa hannun daman Israʼila, ya kuma kawo su kusa da shi. 14 Amma
Israʼila ya miƙa hannun damansa ya sa shi a kan Efraim, ko da yake shi ne ƙaramin, ta wurin harɗewa hannuwansa, ya sa hannun hagunsa a kan Manasse, ko da yake Manasse ne ɗan farinsa.

15 Saʼan nan ya albarkaci Yusuf ya ce,

“Bari Allah a gaban wanda kakannina
Ibrahim da Ishaku suka yi tafiya,
Allahn da ya zama makiyayina
dukan raina zuwa wannan rana,
16 Malaʼikan da ya cece ni daga dukan cuta
bari yă albarkaci samarin nan.
Bari a kira su da sunana
da sunayen kakannina Ibrahim da Ishaku
bari kuma su ƙaru ƙwarai
a bisa duniya.”

17 Saʼad da Yusuf ya ga mahaifinsa yana sa hannun damansa a kan Efraim bai ji
daɗi ba; saboda haka ya ɗauke hannun mahaifinsa ya cire shi daga kan Efraim zuwa
kan Manasse. 18 Yusuf ya ce masa, “Aʼa, mahaifina, wannan shi ne ɗan farin; ka sa hannunka na dama a kansa.”

19 Amma mahaifinsa ya ƙi ya ce, “Na sani, ɗana, na sani. Shi ma zai zama mutane,
zai kuma zama mai girma. Duk da haka ɗanʼuwansa zai zama mai girma fiye da shi,
kuma zuriyarsa za tă zama ƙungiyar alʼummai.” 20 Ya albarkace su a wannan rana
ya ce,

“A cikin sunanku Israʼila zai sa wannan albarka
ʻBari Allah yă sa ku zama kamar Efraim da Manasse.ʼ ”

Saboda haka ya sa Efraim gaban Manasse.

21 Saʼan nan Israʼila ya ce wa Yusuf, “Ina gab da mutuwa, amma Allah zai kasance
tare da ku 22 Kuma gare ka, a matsayi wanda yake kan ʼyanʼuwanka, na ba da gonar
da na karɓe daga Amoriyawa da takobi da kuma bakana.”

# 49

### *Yaƙub ya albarkaci ʼyaʼyansa maza*

1 Sai Yaƙub ya kira ʼyaʼyansa maza ya ce, “Ku tattaru don in faɗa muku abin da zai faru gare ku, a kwanaki masu zuwa.

2 “Ku tattaru, ku saurara, ʼyaʼyan Yaƙub maza;
ku saurari mahaifinku, Israʼila.

3 “Ruben, kai ne ɗan farina,

ƙarfina, alamar farko ta ƙarfina,
mafi matsayi, kuma mafi iko.
4 Mai tumbatsa kamar ruwa, amma ba za ka ƙara zama mai daraja ba,
gama ka hau gadon mahaifinka
ka hau kujerata, ka kuma ƙazantar da shi.

5 “Simeyon da Lawi ’yan’uwa ne,
takubansu makamai ne na tā da hankali.
6 Ba zan shiga shawararsu ba,
ba zan shiga taronsu ba,
gama sun kashe maza cikin fushinsu
cikin ganin dama suka kashe bijimai.
7 La’ananne ne fushinsu, mai tsanani ne ƙwarai,
hasalarsu kuwa, muguwa ce ƙwarai!
Zan warwatsa su cikin Yaƙub
in kuma daidaita su cikin Isra’ila.

8 “Yahuda,* ’yan’uwanka za su yabe ka;
hannuwanka za su kasance a wuyan abokan gābanka,
’ya’yan mahaifinka maza za su rusuna maka.
9 Kai ɗan zaki ne, ya Yahuda,
ka dawo daga farauta, ɗana.
Kamar zaki, yakan kwanta a miƙe,
kamar zakanya, wa yake da ƙarfin halin tashe shi?
10 Kursiyi ba zai tashi daga Yahuda ba,
ba kuwa sandan mulki daga tsakani ƙafafunsa ba,
sai ya zo ga wanda yake mai shi†.
Biyayyar al’umma kuwa tasa ce.
11 Zai daure jakinsa a kuringa,
aholakinsa a rassa mafi kyau;
zai wanke tufafinsa cikin ruwan inabi
rigunansa cikin inabi ja wur kamar jini.
12 Idanunsa za su duhunce fiye da ruwan inabi,
haƙorarsa farare kamar madara.‡

13 “Zebulun zai zauna a bakin teku,
yă zama tasar jiragen ruwa;
iyakarsa za tă nausa zuwa Sidon.

14 “Issakar doki§ mai ƙarfi,
kwance tsakanin buhunan sirdi.*
15 Sa’ad da ya ga yadda wurin hutunsa yana da kyau
da kuma daɗin da ƙasarsa take,
zan tanƙware kafaɗarsa ga nauyi
yă miƙa kai ga aikin dole.

16 “Dan† zai tanada adalci wa mutanensa
kamar ɗaya cikin kabilan Isra’ila.

---

* **49:8** Yahuda ya yi kamar ya fito daga Ibraniyanci na yabo ne. † **49:10** Ko kuwa sai Shilo ya zo; ko kuwa sai ya zo ga girma ya dace. ‡ **49:12** Ko kuwa zai zama marar walƙiya daga ruwan inabi, haƙorarsa farare daga madara § **49:14** Ko kuwa mai ƙarfi * **49:14** Ko kuwa sansanin wuta † **49:16** Dan a nan yana nufin yakan tanada adalci.

17 Dan zai zama maciji a gefen hanya,
kububuwa a bakin hanya,
da take saran ɗiɗɗigen doki
domin mahayinsa yă fāɗi da baya.

18 “Ina zuba ido ga cetonka, ya UBANGIJI.

19 “Masu fashi za su fāɗa wa Gad,‡
amma zai runtume su.

20 “Abincin Asher zai zama a wadace,
zai yi tanadin abinci iri-iri da suka dace don sarki.

21 “Naftali sakakkiyar barewa ce
da take haihuwar kyawawan ’ya’ya.§

22 “Yusuf kuringa ce mai ba da amfani.
Kuringa mai ba da amfani kusa da rafi
wadda rassanta na hawan bango.*
23 Da ɗaci rai mahara suka fāɗa masa;
suka harbe shi babu tausayi.
24 Amma bakansa yana nan daram
hannuwansa masu ƙarfi ba sa jijjiguwa†
saboda hannun Maɗaukaki na Yaƙub,
saboda Makiyayi, Dutsen Isra’ila,
25 saboda Allah na mahaifinka, wanda ya taimake ka,
saboda Maɗaukaki,‡ wanda yake albarkace ka
da albarkar sama da take bisa
albarkun zurfafa da suke ƙarƙashin ƙasa
albarkun mama da kuma mahaifa.
26 Albarkun mahaifi suna da girma fiye
da albarkun daɗaɗɗun duwatsu
fiye§ da yalwar madawwaman tuddai.
Bari dukan waɗannan su zauna a kan Yusuf,
a goshin ɗan sarki a cikin* ’yan’uwansa.

27 “Benyamin kyarkeci ne mai kisa;
da safe yakan cinye abin da ya farauto
da yamma yakan raba ganima.”
28 Dukan waɗannan su ne kabilu goma sha biyu na Isra’ila, kuma abin da
mahaifinsu ya faɗa musu ke nan sa’ad da ya albarkace su, yana ba kowane albarkar
da ta dace da shi.

### *Mutuwar Yaƙub*

29 Sa’an nan ya ba su waɗannan umarnai ya ce, “Ina gab da a tara ni ga mutanena.
Ku binne ni tare da kakannina a kogon da yake cikin filin Efron mutumin Hitti,
30 kogon da yake cikin filin Makfela, kusa da Mamre a Kan’ana, wanda Ibrahim ya
saya tare da filin, yă zama makabarta daga Efron mutumin Hitti. 31 A can aka binne

‡ **49:19** Gad na iya nufin fāɗawa da kuma ƙungiyar mahara. § **49:21** Ko kuwa yakan faɗa kyawawan kalmomi * **49:22** Ko kuwa Yusuf aholakin jeji ne, aholakin jeji kusa da rafi, jakin jeji a tudun mai kunyoyi † **49:24** Ko kuwa mahara za su fāɗa, za su harba, za su rage, za su tsaya ‡ **49:25** Da Ibraniyanci Shaddai § **49:26** Ko kuwa kakana, mai girma kamar * **49:26** Ko kuwa wanda aka raba da

Ibrahim da matarsa Saratu, a can aka binne Ishaku da matarsa Rebeka, a can kuma
na binne Liyatu. 32 Filin tare da kogon da yake ciki, an saya daga Hittiyawa."†
33 Sa'ad da Yaƙub ya gama ba da umarnan ga 'ya'yansa maza, sai ya ɗaga ƙafafunsa
zuwa gado, ya ja numfashinsa na ƙarshe, aka kuwa tara shi ga mutanensa.

# 50

1 Yusuf kuwa ya fāɗa a kan mahaifinsa, ya yi kuka a kansa, ya kuma sumbace
shi. 2 Sa'an nan Yusuf ya umarci masu maganin da suke yin masa hidima, su shafe
mahaifinsa Isra'ila da maganin hana ruɓa. Saboda haka masu maganin suka shafe
shi da maganin hana ruɓa. 3 Suka ɗauki kwana arba'in cif suna yin wannan, gama
kwanakin da ake bukata ke nan don shafewa da maganin hana ruɓa. Masarawa
kuwa suka yi makoki dominsa kwana saba'in.
4 Sa'ad da kwanakin makoki suka wuce, sai Yusuf ya ce wa iyalin gidan Fir'auna,
"In na sami tagomashi a idanunku, ku yi magana da Fir'auna domina. Ku faɗa masa,
5 'Mahaifina ya sa na yi rantsuwa, ya kuma ce, "Ina gab da mutuwa, ka binne ni a
kabarin da na haƙa wa kaina a ƙasar Kan'ana." Yanzu fa bari in haura in binne
mahaifina, sa'an nan in dawo.' "
6 Fir'auna ya ce, "Haura ka binne mahaifinka, kamar yadda ya sa ka rantse za ka
yi."
7 Saboda haka Yusuf ya haura don yă binne mahaifinsa. Dukan hafsoshin Fir'auna
suka yi masa rakiya tare da manyan mutanen gidan Fir'auna, da kuma dukan
manyan mutanen Masar 8 da kuma dukan membobin gidan Yusuf, da 'yan'uwansa
da kuma waɗanda suke na gidan mahaifinsa. Yara kaɗai da garkunansu da kuma
shanunsu ne aka bari a Goshen. 9 Kekunan yaƙi da mahayan dawakai* su ma suka
haura tare da shi. Babbar ƙungiya jama'a ce ƙwarai.
10 Sa'ad da suka kai masussukar Atad, kusa da Urdun, sai suka yi kuka da ƙarfi da
kuma mai zafi, a can Yusuf ya yi makoki kwana bakwai saboda mahaifinsa. 11 Sa'ad
da Kan'aniyawa waɗanda suke zama a can suka ga makokin a masussukan Atad, sai
suka ce, "Masarawa suna bikin makoki na musamman." Shi ya sa ake kira wannan
wurin da yake kusa da Urdun, Abel-Mizrayim.†
12 Haka fa 'ya'yan Yaƙub maza suka yi yadda ya umarce su. 13 Suka ɗauke shi
zuwa ƙasar Kan'ana suka kuma binne shi a kogon da yake cikin filin Makfela, kusa
da Mamre, wanda Ibrahim ya saya tare da filin, ya zama makabarta daga Efron
mutumin Hitti. 14 Bayan ya binne mahaifinsa, sai Yusuf ya koma Masar, tare da
'yan'uwansa da kuma dukan waɗanda suka tafi tare da shi don binne mahaifinsa.

### *Yusuf ya sāke ba wa 'yan'uwansa tabbaci*

15 Sa'ad da 'yan'uwan Yusuf suka ga cewa mahaifinsu ya mutu, sai suka ce, "Mai
yiwuwa Yusuf yana riƙe da mu a zuciya, wataƙila zai rama dukan abubuwa marasa
kyau da muka yi masa?" 16 Saboda haka suka aika wa Yusuf suna cewa, "Mahaifinka
ya bar waɗannan umarnai kafin yă rasu. 17 Ga abin da za ku ce wa Yusuf, 'Na roƙe ka,
ka gafarta wa 'yan'uwanka zunubai da laifofin da suka aikata na abubuwa marasa
kyau da suka yi maka.' Yanzu muna roƙonka ka gafarta zunuban bayin Allah na
mahaifinka." Sa'ad da saƙonsu ya zo masa, sai Yusuf ya yi kuka.
18 'Yan'uwansa kuwa suka zo suka fāɗi a gabansa suka ce, "Mu bayinka ne."
19 Amma Yusuf ya ce musu, "Kada ku ji tsoro. Ni Allah ne? 20 Kun yi niyya ku yi
mini lahani, amma Allah ya nufe wannan ya zama alheri don yă cika abin da yanzu
yake faruwa, ceton rayuka masu yawa. 21 Saboda haka, kada ku ji tsoro. Zan tanada

---

† **49:32** Ko kuwa 'ya'ya mazan Het * **50:9** Ko kuwa mahayan kekunan yaƙi † **50:11** Abel-Mizrayim yana nufin makokin Masarawa.

muku da kuma ʼyaʼyanku.” Ya sāke tabbatar musu, ya kuma yi musu magana ta alheri.

### *Mutuwar Yusuf*

22 Yusuf ya zauna a Masar tare da dukan iyalin mahaifinsa. Ya rayu shekara ɗari
da goma. 23 Ya kuma ga tsara ta uku ta ʼyaʼyan Efraim. Haka ma ʼyaʼyan Makir ɗan
Manasse, an haife su aka sa a gwiwoyin Yusuf.‡
24 Sai Yusuf ya ce wa ʼyanʼuwansa, “Ina gab da mutuwa. Amma tabbatacce Allah zai
taimake ku, yă fid da ku daga wannan ƙasa zuwa ƙasar da ya alkawarta da rantsuwa
wa Ibrahim, Ishaku da kuma Yaƙub.” 25 Yusuf kuwa ya sa ʼyaʼyan Israʼila maza suka
yi rantsuwa, ya kuma ce, “Tabbatacce Allah zai taimake ku, ku kuma dole ku ɗauki
ƙasusuwana, ku haura da su daga wannan wuri.”
26 Yusuf kuwa ya rasu yana da shekara ɗari da goma. Bayan an shafe shi da
maganin hana ruɓa, sai aka sa shi a akwatin gawa a Masar.

‡ **50:23** Wato aka ɗauka su kamar nasa.

# Fitowa

*Wahalar Isra'ilawa a Masar*

1 Waɗannan su ne sunayen 'ya'yan Isra'ila maza, waɗanda suka tafi Masar
tare da Yaƙub; kowanne da iyalinsa.

2 Ruben, Simeyon, Lawi da Yahuda;
3 Issakar, Zebulun da Benyamin;
4 Dan da Naftali;
Gad da Asher.

5 Zuriyar Yaƙub duka sun kai mutum saba'in. Yusuf ya riga ya kasance a
Masar.

6 Yanzu Yusuf da dukan 'yan'uwansa da kuma dukan tsaran nan da suka tafi Masar,
sun mutu, 7 amma Isra'ilawa sun riɓaɓɓanya, suka kuma yi ta haihuwa sosai, suka
yi yawan sosai, har ƙasar ta cika da su.
8 Sai wani sabon sarki wanda bai san Yusuf ba, ya hau sarautar Masar. 9 Ya ce wa
mutanensa, "Duba Isra'ilawa sun yi yawa, sun fi ƙarfinmu. 10 Ku zo, mu yi dabara a
kansu, in ba haka ba za su ƙaru fiye da haka, in kuwa yaƙi ya tashi tsakaninmu da
abokan gāba, za su iya haɗa kai da abokan gāba, su yaƙe mu, su bar ƙasar."
11 Saboda haka sai suka naɗa shugabannin gandu a kansu don su wahalshe su, su
kuma bauta musu, suka sa su suka gina biranen Fitom da Rameses su zama biranen
ajiya, domin Fir'auna. 12 Amma duk da wannan ƙarin wulaƙancin da ake yi musu,
su kuwa sai daɗa riɓaɓɓanya suke ta yi. Sai tsoron Isra'ilawa ya ƙaru a zuciyar
Masarawa, 13 ganin haka sai Masarawa suka ƙara musu wahala. 14 Suka baƙanta
wa Isra'ilawa rai da bauta mai wuya, ta wurin sa su yin tubali da yumɓu, da kuma
kowace irin bauta a gonaki. A cikin dukan ayyukansu, Masarawa ba su ji tausayinsu
ba ko kaɗan.
15 Sai Sarkin Masar ya gaya wa ungozomomin matan Ibraniyawa, wato, su Shofra da
Fuwa ya ce, 16 "Sa'ad da kuke taimakon matan Ibraniyawa lokacin haihuwa, in jaririn
namiji ne ku kashe shi, amma in ta mace ce, ku bar ta da rai." 17 Amma ungozomomin
nan masu tsoron Allah ne, ba su kuwa aikata abin da sarkin Masar ya gaya musu ba;
suka bar jarirai maza su rayu. 18 Sai sarkin Masar ya kira ungozomomin, ya tambaye
su ya ce, "Don me kuka yi haka? Don me kuka bar jarirai maza su rayu?"
19 Ungozoman suka amsa wa Fir'auna suka ce, "Ai, matan Ibraniyawa ba kamar
matan Masarawa ba ne, gwarzaye ne, sukan haihu kafin ungozomomin su kai
wurinsu."
20 Saboda haka Allah ya nuna alheri wa ungozomomin, Isra'ilawa kuwa suka yi
yawa fiye da dā. 21 Saboda ungozomomin suna tsoron Allah, sai Allah ya ba su iyalan
kansu.
22 Sai Fir'auna ya ba da umarni wa mutanensa ya ce, "Duk yaron da yake namijin
da haka haifa, dole ku jefa shi cikin kogi, amma ku bar yara mata su rayu."

# 2

*Haihuwar Musa*

1 Ana nan, sai wani Balawe ya auri wata Balawiya, 2 ta kuwa yi ciki, ta haifi ɗa.
Sa'ad da ta ga jaririn kyakkyawa ne, sai ta ɓoye shi har watanni uku. 3 Amma da
ba tă iya ɓoye shi kuma ba, sai ta yi kwandon kyauro ta shafa masa kwalta. Bayan

haka sai ta sa jaririn a cikin kwandon, ta je ta ajiye kwandon tare da jaririn a cikin
kyauro, a bakin kogin. 4 ’Yar’uwarsa ta tsaya da ɗan rata tana lura da abin da zai
faru da shi.
5 Sai ’yar Fir’auna ta gangara zuwa kogi domin tă yi wanka, bayinta kuwa suna
tafiya a bakin kogi. Sai ta ga kwandon a ciyawa, ta aiki ɗaya daga cikin masu
hidimarta tă ɗauko mata. 6 Da ta buɗe kwandon, sai ta ga yaro yana kuka, ta kuwa
ji tausayinsa. Ta ce, “Wannan ɗaya daga cikin jariran Ibraniyawa ne.”
7 Sai ’yar’uwarsa ta tambayi ’yar Fir’auna, ta ce, “In tafi in samo ɗaya daga cikin
matan Ibraniyawa tă yi miki renon yaron?”
8 Sai ta amsa ta ce, “I, tafi.” Sai yarinyar ta tafi ta kawo mahaifiyar yaron. 9 Diyar
Fir’auna ta ce mata, “Ɗauki jaririn, ki yi mini renonsa, zan kuwa biya ki.” Saboda
haka ta ɗauki yaron, ta yi renonsa. 10 Sa’ad da ya yi girma, sai ta kawo shi wajen ’yar
Fir’auna, ya kuwa zama ɗanta, ta kuma ba shi suna Musa, tana cewa, “Na tsamo shi
daga ruwa.”

*Musa ya gudu zuwa Midiyan*

11 Wata rana, bayan Musa ya yi girma, sai ya haura, ya tafi inda mutanensa suke,
ya kuma ga yadda suke shan wahala da aiki. Ya ga wani mutumin Masar yana dūkan
mutumin Ibraniyawa, ɗaya daga cikin mutanensa. 12 Da ya leƙa nan da can bai kuwa
ga kowa ba, sai ya kashe mutumin Masar, ya ɓoye shi a yashi. 13 Kashegari ya fita, sai
ya ga Ibraniyawa biyu suna faɗa. Ya tambayi mai laifin ya ce, “Don me kake bugun
ɗan’uwanka, mutumin Ibraniyawa?”
14 Mutumin ya ce masa, “Wa ya mai da kai mai mulki da mai hukunci a kanmu?
Kana so ne ka kashe ni kamar yadda ka kashe mutumin Masar nan?” Sai Musa ya
tsorata, ya yi tunani ya ce, “To, fa, abin nan da na yi, ya zama sananne.”
15 Da Fir’auna ya ji wannan, sai ya yi ƙoƙari yă kashe Musa, amma Musa ya gudu
daga wajen Fir’auna, ya tafi ƙasar Midiyan inda ya zauna kusa da wata rijiya. 16 To,
fa, akwai wani firist na Midiyan, yana da ’ya’ya mata bakwai, suka zo su shayar da
dabbobin mahaifinsu. 17 Sai waɗansu makiyaya suka zo suka kore su, amma Musa
ya tashi ya taimake su ya shayar da dabbobinsu.
18 Da ’yan matan suka komo wurin Reyuwel mahaifinsu, sai ya tambaye su ya ce,
“Yaya kuka dawo da wuri yau?”
19 Suka amsa suka ce, “Wani mutumin Masar ne ya taimake mu daga hannun
waɗansu makiyaya. Har ma ya ɗebo ruwa ya shayar da dabbobin.”
20 Ya tambayi ’yan matansa, “To ina yake? Don me kuka bar shi a can? A gayyace
shi, yă zo, yă ci wani abu.”
21 Musa ya yarda yă zauna da mutumin wanda ya ba da ’yarsa Ziffora aure da
Musa. 22 Ziffora ta haifi wa Musa ɗa, ya kuma raɗa masa suna Gershom cewa, “Na
zama baƙo a baƙuwar ƙasa.”
23 Ana nan dai, a kwana a tashi, sai sarkin Masar ya mutu. Isra’ilawa suka yi kuka
mai zafi saboda bautarsu mai wuya, sai kukar neman taimakonsu saboda bauta, ya
kai wurin Allah. 24 Allah kuwa ya ji kukansu sai ya tuna da alkawarinsa da Ibrahim
da Ishaku da Yaƙub. 25 Sai Allah ya dubi Isra’ilawa, ya kuma damu da su.

# 3

*Musa da ƙaramin itace mai cin wuta*

1 Ana nan wata rana Musa yana kiwon tumakin Yetro surukinsa, firist na Midiyan,
sai ya bi da tumaki zuwa gefe mai nisa a cikin hamada, har ya zo Horeb, dutsen Allah.
2 A can mala’ikan Ubangiji ya bayyana a gare shi cikin harshen wuta, a ƙaramin itace.
Musa ya lura cewa ko da yake wuta na ci ƙaramin itacen, amma bai ƙone ba. 3 Sai

Musa ya ce, “Wannan abin mamaki ne, don me wannan itace bai ƙone ba? Bari in
matso kusa in gani.”

4 Da UBANGIJI ya ga Musa ya matso don yǎ duba, sai Allah ya yi kira daga cikin
ƙaramin itacen ya ce, “Musa! Musa!”

Sai Musa ya amsa ya ce, “Ga ni.”

5 Allah ya ce, “Kada ka zo kusa, tuɓe takalmanka, gama inda kake tsaye, wuri ne
mai tsarki.” 6 Sai Allah ya ce, “Ni ne Allah na kakanninka, Allah na Ibrahim, Allah na
Ishaku da kuma Allah na Yaƙub.” Da jin wannan, sai Musa ya ɓoye fuskarsa, domin
ya ji tsoro yǎ dubi Allah.

7 UBANGIJI ya ce, “Tabbatacce na ga azabar mutanena a Masar. Na ji su suna kuka
saboda matsin da shugabannin gandunsu suke musu, na kuma damu da wahalarsu.
8 Saboda haka na sauko domin in cece su daga hannun Masarawa, in kuma fitar da su
daga ƙasar Masar, in kai su ƙasa mai kyau mai fāɗi, ƙasa mai zub da madara da zuma,
inda Kan’aniyawa, Hittiyawa, Amoriyawa, Ferizziyawa, Hiwiyawa da Yebusiyawa
suke. 9 Yanzu kukan Isra’ilawa ya kai gare ni, na kuma ga yadda Masarawa suke
wulaƙanta su 10 To, fa, sai ka tafi. Ina aikan ka wurin Fir’auna don ka fitar da
mutanena Isra’ilawa daga Masar.”

11 Amma Musa ya ce wa Allah, “Wane ni in tafi wurin Fir’auna, in kuma fitar da
Isra’ilawa daga Masar?”

12 Sai Allah ya ce, “Zan kasance da tare kai. Wannan kuwa za tǎ zama alama a gare
ka cewa Ni na aike ka. Bayan ka fitar da mutanen daga Masar, za ku yi sujada ga
Allah a kan dutsen nan.”

13 Musa ya ce wa Allah, “A ce ma na tafi wurin Isra’ilawa na ce musu, ‘Allah na
kakanninku ya aiko ni wurinku,’ in suka tambaye ni, ‘Mene ne sunansa?’ Me zan
ce?”

14 Allah ya ce wa Musa, “NI NE wanda NINE. Abin da za ka faɗa wa Isra’ilawa ke
nan cewa, ‘NI NE, ya aiko ni wurinku.’ ”

15 Allah ya kuma ce wa Musa, “Ka faɗa wa Isra’ilawa, ‘UBANGIJI, Allah na
kakanninka, Allah na Ibrahim, Allah na Ishaku da kuma Allah na Yaƙub, ya aiko
ni wurinku.’ Wannan shi ne sunana har abada, sunan da za a tuna da ni daga tsara
zuwa tsara ke nan.

16 “Tafi ka tattara dattawan Isra’ila, ka ce musu, ‘UBANGIJI, Allah na kakanninku,
Allah na Ibrahim, Ishaku da Yaƙub, ya bayyana a gare ni ya ce, Na lura da ku, na kuma
ga abubuwan da ake yi muku a Masar. 17 Na kuma yi alkawari, zan fitar da ku daga
azabarku a Masar zuwa ƙasar Kan’aniyawa, Hittiyawa, Amoriyawa, Ferizziyawa,
Hiwiyawa da Yebusiyawa, ƙasa mai zub da madara da zuma.’

18 “Dattawan Isra’ila za su saurare ka. Sa’an nan da kai da dattawan Isra’ila, za ku
tafi wurin sarkin Masar, ku ce masa, ‘UBANGIJI, Allah na Ibraniyawa, ya sadu da mu.
Bari mu yi tafiyar kwana uku zuwa cikin hamada domin mu yi hadaya wa UBANGIJI
Allahnmu.’ 19 Amma na san cewa sarkin Masar ba zai yarda ku tafi ba, sai hannu
mai ƙarfi ya tilasta shi. 20 Saboda haka zan miƙa hannuna in bugi Masarawa da duk
al’ajaban da zan aikata a cikinsu. Bayan haka zai bar ku, ku tafi.

21 “Zan kuma sa mutanen su sami tagomashi daga wurin Masarawa, saboda sa’ad
da za ku fita, ba za ku fita hannu wofi ba. 22 Kowace mace ta tambayi maƙwabciyarta,
da kuma duk wata macen da take cikin gidanta, kayayyakin azurfa da na zinariya da
kuma na riguna, waɗanda za ku sa wa ’ya’yanku maza da mata. Ta haka nan za ku
washe Masarawa.”

# 4

*Mu’ujizai domin Musa*

1 Musa ya amsa ya ce, “In ba su gaskata ni ba, suka kuma ce, ‘Ubangiji bai bayyana
gare ka ba fa’?”

2 Sai Ubangiji ya ce, “Mene ne wannan a hannunka?”

Musa ya amsa ya ce, “Sanda.”

3 Sai Ubangiji ya ce, “Jefa shi ƙasa.”

Musa ya jefa shi ƙasa, sai sandan ya zama maciji, Musa kuwa ya gudu daga gare
shi. 4 Sai Ubangiji ya ce masa, “Sa hannunka ka ɗauke shi ta wutsiya.” Sai Musa ya
miƙa hannu, ya kama macijin, macijin kuwa ya dawo sanda a hannunsa. 5 Ubangiji
ya ce, “Wannan zai sa su ba da gaskiya cewa Ubangiji, Allah na kakanninsu, Allah
na Ibrahim, Allah na Ishaku, da kuma Allah da Yaƙub, ya bayyana gare ka.”

6 Sa’an nan Ubangiji ya ce, “Sa hannunka cikin rigarka.” Sai Musa ya sa hannunsa
cikin rigarsa, sa’ad da ya fitar da shi, sai hannun ya a kuturce fari fat, kamar ƙanƙara.

7 Sai Ubangiji ya ce, “Yanzu, mayar da hannunka a rigarka.” Sai Musa ya sa
hannunsa cikin rigarsa, da ya fitar da shi, sai hannun ya koma kamar sauran jikinsa.

8 Sa’an nan Ubangiji ya ce, “In ba su gaskata ba, ko kuma ba su kula da mu’ujiza ta
fari ba, wataƙila su gaskata da ta biyun. 9 Amma in ba su gaskata mu’ujizan nan biyu
ba, ko kuwa ba su saurare ka ba, sai ka ɗibo ruwa daga Nilu, ka zuba a busasshiyar
ƙasa. Ruwan da ka ɗebo daga kogin zai zama jini a ƙasar.”

10 Musa ya ce wa Ubangiji, “Ya Ubangiji, ni ban mai iya magana ba ne, ban taɓa
iya ba, ko a yanzu ma, bayan ka yi magana da ni, gama ni mai nauyin baki ne, mai
nauyin harshe kuma.”

11 Ubangiji ya ce masa, “Wa ya ba mutum bakinsa? Wa yake maishe shi kurma ko
bebe? Wa yake ba shi gani ko yă makanta shi? Ashe ba Ni Ubangiji ba ne? 12 Yanzu
tafi, zan taimake ka ka yi magana, zan kuma koya maka abin da za ka faɗa.”

13 Amma Musa ya ce, “Ya Ubangiji, ina roƙonka, ka nemi wani ka aika.”

14 Sai Ubangiji ya yi fushi da Musa ya ce, “Ɗan’uwanka Haruna Balawe, ba ya nan
ne? Na san ya iya magana. Ya riga ya kama hanya don yă sadu da kai, zai kuma yi
farin ciki sa’ad da ya gan ka. 15 Za ka yi masa magana. Ka kuma sa masa maganata a
baki; zan kuma taimake ku magana, in koya muku abin da za ku yi. 16 Zai yi magana
da mutane a madadinka, zai zama kamar bakinka, kai kuwa kamar Allah a gare shi.
17 Amma ka ɗauki wannan sanda a hannunka domin yă aikata mu’ujizan.”

### *Musa ya koma Masar*

18 Sai Musa ya koma wurin Yetro surukinsa, ya ce masa, “Bari in koma wurin
mutanena a Masar, in ga ko da mai rai a cikinsu.”

Yetro ya ce, “Tafi, ka kuma sauka lafiya.”

19 Ubangiji ya riga ya gaya wa Musa a Midiyan, “Koma Masar, domin dukan
mutanen da suke neman su kashe ka sun mutu.” 20 Sai Musa ya ɗauki matarsa da
’ya’yansa maza, ya sa su a kan jaki, suka kama hanya zuwa Masar. Ya kuma ɗauki
sandan Allah a hannunsa.

21 Ubangiji ya ce wa Musa, “Bayan ka koma Masar, ka tabbata ka aikata dukan
mu’ujizan da na sa cikin ikonka a gaban Fir’auna. Amma zan taurare zuciyarsa
domin kada yă bar mutanen su tafi. 22 Sa’an nan ka gaya wa Fir’auna, ‘Ga abin da
Ubangiji ya ce; Isra’ila shi ne ɗan farina, 23 na gaya maka, “Ka bar ɗana yă tafi domin
yă yi mini sujada.” Amma ka ƙi ka bari yă tafi, saboda haka zan kashe ɗan farinka.’ ”

24 Ya zama kuwa sa’ad da Musa yake masauki a kan hanya sai Ubangiji ya gamu da
shi, ya nema ya kashe shi. 25 Amma Ziffora ta ɗauki dutsen ƙanƙara mai ci, ta yanke
loɓar ɗanta ta taɓa ƙafafun Musa da shi. Ta ce, “Tabbatacce kai angon jini ne a gare
ni.” 26 Sai Ubangiji ya ƙyale shi. (A lokacin ta ce “angon jini,” tana nufin kaciya.)

27 Ubangiji ya ce wa Haruna, “Tafi cikin hamada ka sadu da Musa.” Sai ya sadu da
Musa a dutsen Allah, ya sumbace shi. 28 Sai Musa ya gaya wa Haruna dukan abin da
Ubangiji ya aike yă faɗa, da kuma dukan mu’ujizan da ya umarce shi yă aikata.
29 Musa da Haruna suka tattara dukan dattawan Isra’ilawa, 30 sai Haruna ya gaya
musu dukan abin da Ubangiji ya ce wa Musa. Ya kuma aikata mu’ujizan a gaban
mutanen, 31 sai suka gaskata. Sa’ad da suka ji cewa Ubangiji ya damu da su, ya kuma
ga azabarsu, sai suka durƙusa suka yi sujada.

# 5

*Yin tubalai ba tare da an ba da bunnu ba*

1 Daga bisani sai Musa da Haruna suka tafi wurin Fir’auna suka ce, “Ga abin da
Ubangiji, Allah na Isra’ila ya ce, ‘Bari mutanena su tafi domin su yi mini biki a
hamada.’ ”
2 Fir’auna ya ce, “Wane ne Ubangiji da zan yi biyayya da shi, har in bar Isra’ila su
tafi? Ban san Ubangiji ba, kuma ba zan bar Isra’ila su tafi ba.”
3 Sai suka ce, “Allah na Ibraniyawa ya sadu da mu. Yanzu bari mu ɗauki tafiyar
kwana uku cikin hamada domin mu miƙa hadaya ga Ubangiji Allahnmu, don kada
yă buga mu da annoba ko takobi.”
4 Amma sarkin Masar ya ce wa, “Musa da Haruna, don me kuke hana mutane yin
aikinsu? Ku koma wurin aikinku!” 5 Sa’an nan Fir’auna ya ce, “Ga shi mutane sun
yi yawa a ƙasar Masar, ku kuma yanzu kuna so ku hana su yin aiki.”
6 A wannan rana Fir’auna ya ba da wannan umarni wa shugabannin masu gandu,
7 “Kada ku ƙara ba wa mutanen ciyawar tattaka domin su yi tubula, bari su tafi su
tattara tattaka da kansu. 8 Ku kuma bukace su su yi tubula daidai yawan tubalin da
suka saba yi, kada ku rage. Ragwaye ne, shi ya sa suke kuka cewa, ‘Bari mu tafi mu
yi hadaya ga Allahnmu.’ 9 Ku sa waɗannan mutane su yi aiki mai tsanani sosai, don
kada su sami zarafin kasa kunne ga maganganun ƙarya.”
10 Sai shugabannin masu aikin gandu suka fita suka gaya wa mutanen Isra’ila, “Ga
abin da Fir’auna ya ce, ‘Ba zan ƙara ba ku tattaka ba. 11 Ku tafi ku nemo wa kanku
tattaka duk inda za ku samu, amma ba za a rage aikinku ba ko kaɗan.’ ” 12 Saboda
haka mutane suka warwatsu ko’ina a Masar domin tattara bunnun da za su yi amfani
da su, maimakon tattaka. 13 Shugabannin gandu suka dinga matsa musu suna cewa,
“Ku cika aikin da aka bukace ku na kowace rana kamar yadda kuke yi sa’ad da kuke
da tattaka.” 14 Manyan Isra’ilawa waɗanda shugabannin gandun Fir’auna suka naɗa,
suka sha dūka, aka kuma yi musu tambayoyi ana cewa, “Don me ba ku cika yawan
tubula na jiya da na yau kamar yadda kuka saba ba?”
15 Sai manyan Isra’ila masu bi da aikin gandu suka tafi wurin Fir’auna suka yi
roƙo suna cewa, “Don me kake yi wa bayinka haka? 16 Ba a ba wa bayinka tattaka,
duk da haka ana ce mana, ‘Ku yi tubula!’ Ana wa bayinka dūka, amma fa laifin na
mutanenka ne.”
17 Fir’auna ya ce, “Ku ragwaye ne! Shi ya sa kuke cewa, ‘Bari mu tafi mu yi hadaya
wa Ubangiji.’ 18 Ku ɓace yanzu daga nan, ku koma wurin aikinku. Ba za a ba ku
tattaka ba, kuma dole ku fid da tubula kamar yadda kuka saba.”
19 Manyan Isra’ilawa da suke bi da aikin gandu suka gane cewa sun shiga uku, sa’ad
da aka gaya musu, “Ba za ku rage yawan tubulan da aka bukace ku ku yi na kowace
rana ba.” 20 Da suka bar Fir’auna, sai suka sadu da Musa da Haruna suna jira su
sadu da su, 21 sai suka ce, “Bari Ubangiji yă duba, yă kuma hukunta ku! Kun maishe
mu abin ƙyama ga Fir’auna da bayinsa, kuka kuma sa musu takobi a hannunsu don
su kashe mu.”

*Allah ya yi alkawarin ceto*

22 Musa ya koma wurin UBANGIJI ya ce, "Ya Ubangiji, don me ka kawo wahala a
kan mutanen nan? Abin da ya sa ka aiko ni ke nan? 23 Gama tun da na tafi wurin
Fir'auna, na yi masa magana da sunanka, sai ya fara gasa wa mutanen nan azaba,
ba ka kuma ceci mutanenka."

## 6

1 Sa'an nan UBANGIJI ya ce wa Musa, "Yanzu za ka gan abin da zan yi da Fir'auna.
Zan sa shi dole yă bar su su tafi, har ma yă iza ƙyeyarsu don su bar ƙasarsa!"
2 Allah ya kuma ce wa Musa, "Ni ne UBANGIJI. 3 Na bayyana ga Ibrahim, ga Ishaku
da kuma ga Yaƙub a matsayin Allah Maɗaukaki, amma sunan nan nawa UBANGIJI,
ban bayyana kaina a gare su ba. 4 Na kuma kafa alkawari da su don in ba su ƙasar
Kan'ana, inda suka yi zaman baƙunci. 5 Ban da haka ma, na ji nishe-nishen Isra'ilawa,
waɗanda Masarawa suka bautar, na kuma tuna da alkawarina.
6 "Saboda haka, ka ce wa Isra'ilawa, 'Ni ne UBANGIJI, zan kuma fitar da ku daga
bauta ta Masarawa. Zan 'yantar da ku daga zama bayinsu, da ƙarfina zan fanshe ku,
in kawo hukunci mai zafi a kansu, don in cece ku. 7 Zan ɗauke ku tamƙar mutanena,
in kuma zama Allahnku. Sa'an nan za ku sani Ni ne UBANGIJI Allahnku, wanda ya
fitar da ku daga wahalar Masarawa. 8 Zan kuwa kawo ku a ƙasar da na rantse da
hannun da na ɗaga sama, cewa zan ba wa Ibrahim, wa Ishaku, da kuma wa Yaƙub.
Zan ba da ita gare ku gādo. Ni ne UBANGIJI.' "
9 Musa ya faɗa wa Isra'ilawa wannan magana, amma ba su kasa kunne a gare shi
ba, don ɓacin rai saboda tsananin aikin bauta.
10 Sa'an nan UBANGIJI ya ce wa Musa, 11 "Koma ka ce wa Fir'auna sarkin Masar, yă
bar Isra'ilawa su fita daga ƙasarsa."
12 Amma Musa ya ce wa UBANGIJI, "In Isra'ilawa ba su ji ni ba, yaya Fir'auna zai ji
ni, da yake ina magana da ƙyar?"

### *Asalin iyalin Musa da Haruna*

13 UBANGIJI ya yi magana da Musa da Haruna game da Isra'ilawa da Fir'auna sarkin
Masar, ya umarce su su fitar da Isra'ilawa daga Masar.

14 Waɗannan su ne shugabannin iyalansu.*

'Ya'yan Ruben maza ɗan farin Isra'ila su ne,
Hanok da Fallu, Hezron da Karmi.
Waɗannan su ne dangin Ruben.

15 'Ya'yan Simeyon maza su ne,
Yemuwel, Yamin, Ohad, Yakin, Zohar da Sha'ul ɗan mutuniyar Kan'ana.
Waɗannan su ne dangin Simeyon.

16 Waɗannan su ne sunayen 'ya'yan Lawi maza bisa ga abin da aka rubuta,
Gershon, Kohat da Merari.
Lawi ya yi shekara 137.
17 'Ya'yan Gershon maza, bisa ga dangi su ne,
Libni da Shimeyi.
18 'Ya'yan Kohat maza, su ne,
Amram, Izhar, Hebron da Uzziyel.
Kohat ya yi shekara 133.
19 'Ya'yan Merari maza, su ne,

* **6:14** Ibraniyanci yana da iyalai ne a nan, aya 25 kuma yana kwatanta babbar ƙungiya fiye da dangi ne.

Mali da Mushi.
Waɗannan su ne dangin Lawi bisa ga abin da aka rubuta.

20 Amram ya auri ’yar’uwar mahaifinsa Yokebed, wadda ta haifa masa Haruna da
Musa.
Amram ya yi shekara 137.
21 ’Ya’yan Izhar maza, su ne,
Kora, Nefeg da Zikri.
22 ’Ya’yan Uzziyel maza, su ne,
Mishayel, Elzafan da Sitri.
23 Haruna ya auri Elisheba, ’yar Amminadab, ’yar’uwar Nashon, sai ta haifa masa
Nadab da Abihu, Eleyazar da Itamar.

24 ’Ya’yan Kora maza, su ne,
Assir, Elkana da Abiyasaf.
Waɗannan su ne dangin Kora.

25 Eleyazar ɗan Haruna, ya auri ɗaya daga cikin ’yan matan Futiyel, sai ta haifa
masa Finehas.

Waɗannan su ne shugabannin iyalan Lawi, dangi, dangi.

26 Wannan Haruna da Musa ne, waɗanda UBANGIJI ya yi musu magana ya ce, “Ku
fitar da Isra’ilawa daga Masar ɓangare-ɓangare.” 27 Su ne suka yi magana da Fir’auna
sarkin Masar game da fitar da Isra’ilawa daga Masar, wannan Musa da Haruna.

### *Haruna zai yi magana a madadin Musa*

28 Ana nan, sa’ad da UBANGIJI ya yi magana da Musa a Masar, 29 ya ce masa, “Ni ne
UBANGIJI. Sai ka faɗa wa Fir’auna sarkin Masar kome da na faɗa maka.”
30 Amma Musa ya ce wa UBANGIJI, “Ni mai nauyin baki ne, ina magana da ƙyar,
ƙaƙa Fir’auna zai kasa kunne gare ni?”

## 7

1 Sai UBANGIJI ya ce wa Musa, “Duba, na maishe ka kamar Allah ga Fir’auna,
ɗan’uwanka Haruna kuma zai zama annabinka. 2 Za ka faɗi kome da na umarce
ka, ɗan’uwanka Haruna kuwa zai faɗa wa Fir’auna, yǎ bar Isra’ilawa su fita daga
ƙasarsa. 3 Amma zan taurare zuciyar Fir’auna, kuma ko da na ninka mu’ujizai da
kuma alamu a Masar, 4 ba zai saurare ku ba. Don haka zan miƙa hannuna a kan
Masar, in murƙushe ta da bala’i iri-iri, bayan haka zan fitar da taron mutanen Isra’ila
daga ƙasar Masar ta wurin hukuntaina masu girma. 5 Masarawa kuwa za su san cewa
ni ne UBANGIJI sa’ad da na miƙa hannuna a kan Masar, na kuma fitar da Isra’ilawa
daga gare ta.”
6 Musa da Haruna suka aikata yadda UBANGIJI ya umarce su. 7 Musa yana da
shekara tamanin da haihuwa, Haruna kuma yana da shekara tamanin da uku, sa’ad
da suka yi magana da Fir’auna.

### *Sandan Haruna ya zama Maciji*

8 UBANGIJI ya ce wa Musa da Haruna, 9 “Sa’ad da Fir’auna ya ce muku, ‘Aikata wani
al’ajabi,’ sai ka ce wa Haruna, ‘Ɗauki sandanka ka jefa shi a ƙasa, a gaban Fir’auna,’
zai kuwa zama maciji.”
10 Sai Musa da Haruna suka tafi wurin Fir’auna, suka yi yadda UBANGIJI ya umarce
su. Haruna ya jefa sandansa ƙasa, a gaban Fir’auna da bayinsa, sai sandan ya zama

maciji. 11 Fir'auna kuwa ya kira masu hikima da masu sihiri, sai bokayen Masarawa
ma suka yi irin abubuwan nan da bokancinsu. 12 Kowannensu ya jefa sandansa ƙasa,
ya kuwa zama maciji. Amma sandan Haruna ya haɗiye sandunansu. 13 Duk da haka
zuciyar Fir'auna ta taurare, bai kuwa saurare su ba, kamar dai yadda UBANGIJI ya
riga ya faɗa.

*Annobar jini*

14 Sa'an nan UBANGIJI ya ce wa Musa, "Zuciyar Fir'auna taurariya ce, ya ƙi yă bar
mutanen su tafi. 15 Ka je wurin Fir'auna da safe, yayinda za shi kogi. Ka jira a bakin
Nilu don ka sadu da shi, ka ɗauki sandan nan da ya canja zuwa maciji a hannunka.
16 Sa'an nan ka ce masa, 'UBANGIJI, Allah na Ibraniyawa, ya aiko ni in faɗa maka, Ka
bar mutanena su tafi domin su yi mini sujada a hamada. Amma har yanzu ba ka yi
biyayya ba. 17 Ga abin da UBANGIJI ya ce, da wannan za ka san cewa ni ne UBANGIJI.
Da sandan da yake hannuna zan bugi ruwan Nilu, zai kuma zama jini. 18 Kifi a ciki
Nilu za su mutu, ruwan kuma zai yi ɗoyi; Masarawa ba za su iya shan ruwansa ba.' "

19 UBANGIJI ya ce wa Musa, "Ka ce wa Haruna, 'Ka ɗauki sandanka, ka miƙa
hannunka kan ruwan Masar, kan kogunansu da rafuffukansu da kududdufansu da
kuma dukan tafkunansu, za su zama jini.' Jini zai kasance ko'ina a Masar, har ma a
cikin abubuwan ajiyar ruwansu* da aka yi da itace da kuma dutse."

20 Musa da Haruna suka yi yadda UBANGIJI ya umarta. Ya ɗaga sandansa a gaban
Fir'auna da bayinsa, ya bugi ruwan Nilu, dukan ruwan kuwa ya zama jini. 21 Kifin
da suke cikin Nilu suka mutu, kogin kuwa ya yi wari sosai yadda Masarawa ba su iya
shan ruwan ba. Jini ya bazu ko'ina a Masar.

22 Amma bokayen Masar ma suka yi abubuwan nan da sihirinsu, sai zuciyar
Fir'auna ta taurare; bai saurari Musa da Haruna ba, kamar dai yadda UBANGIJI ya
riga ya faɗa. 23 A maimakon yă saurara, sai ya juya ya koma fadarsa, bai ma damu
da abin da aka yi ba. 24 Sai dukan Masarawa suka yi ta tonon gefen Nilu don su sami
ruwan sha, domin ba su iya shan ruwan kogin ba.

*Annobar kwaɗi*

25 Kwana bakwai suka wuce bayan da UBANGIJI ya bugi kogin.

# 8

1 Sa'an nan UBANGIJI ya ce wa Musa, "Ka je wurin Fir'auna, ka ce masa, 'Ga abin
da UBANGIJI yana cewa, ka bar mutanena su tafi domin su yi mini sujada. 2 In ka
ƙi barinsu, zan hore ka da annoban kwaɗi a dukan ƙasarka. 3 Nilu zai cika da
kwaɗi. Za su haura zuwa cikin fadanka da kan gadonka, cikin gidajen bayinka da
kan mutanenka, cikin kwanonin toye-toyenka da na cin abincinka. 4 Kwaɗin nan za
su yi ta tsalle a kanka, da kan mutanenka, da kuma kan dukan bayinka.' "

5 Sai UBANGIJI ya ce wa Musa, "Ka ce wa Haruna, 'Ka miƙa hannunka da sandanka
bisa koguna da rafuffuka da kuma kududdufai, ka sa kwaɗi su fito su mamaye ƙasar
Masar.' "

6 Sai Haruna ya miƙa hannunsa bisa ruwan Masar, kwaɗi kuwa suka fito, suka
mamaye ƙasar Masar. 7 Amma bokaye ma suka yi abubuwan nan ta wurin sihirinsu;
suka sa kwaɗi suka fito suka mamaye ƙasar Masar.

8 Fir'auna ya kira Musa da Haruna ya ce, "Yi addu'a ga UBANGIJI yă ɗauke kwaɗi
daga gare ni da mutanena, zan kuwa bar mutanenku su tafi su yi hadaya ga UBANGIJI."

9 Musa ya ce wa Fir'auna, "Na ba ka dama ka ba da lokacin da zan yi addu'a
dominka da kuma bayinka da mutanenka, gidajenku kuwa za su rabu da kwaɗi,
amma ban da waɗanda suke cikin Nilu."

* **7:19** Ko kuwa har ma a kan gumakansu

10 Fir'auna ya ce, "Gobe."
Musa ya amsa, "Za a yi kamar yadda ka faɗa, domin ka sani babu wani kamar
UBANGIJI, Allahnmu. 11 Kwaɗin za su bar ka da gidajenka, bayinka da mutanenka; za
su kasance a Nilu ne kaɗai."
12 Bayan Musa da Haruna sun bar Fir'auna, Sai Musa ya yi kuka ga UBANGIJI saboda
kwaɗin da ya kawo a bisa Fir'auna. 13 Sai UBANGIJI ya yi abin da Musa ya nema.
Kwaɗin suka mutu a gidaje, da filaye, da kuma gonaki. 14 Aka jibga su tsibi-tsibi,
ƙasar ta yi ɗoyi saboda su. 15 Amma da Fir'auna ya ga an sami sauƙi, sai ya taurare,
ya ƙi yă saurari Musa da Haruna kamar dai yadda UBANGIJI ya riga ya faɗa.

### *Annobar ƙwari masu cizo*

16 Sa'an nan UBANGIJI ya ce wa Musa, "Ka ce wa Haruna, 'Miƙa hannunka ka bugi
ƙurar ƙasa,' dukan ƙurar ƙasar Masar kuwa za tă zama ƙwari masu cizo." 17 Suka yi
haka, da Haruna ya miƙa hannunsa da sandan, ya bugi ƙurar ƙasa, sai ƙwari masu
cizo suka fito a kan mutane da dabbobi. Dukan ƙurar, ko'ina a ƙasar Masar ta zama
cinnaku. 18 Sa'ad da bokayen Fir'auna suka yi ƙoƙari yin sihiri iri na rufe ido domin
su fito da kwari, sai suka kāsa.
Kwari masu cizo kuwa suka rufe mutane da dabbobi. 19 Sai bokaye suka ce wa
Fir'auna, "Wannan fa da hannun Allah a ciki." Amma zuciyar Fir'auna ta taurare,
bai kuwa saurara ba, kamar dai yadda UBANGIJI ya riga ya faɗa.

### *Annobar ƙudaje*

20 Sai UBANGIJI ya ce wa Musa, "Ka tashi da sassafe ka sadu da Fir'auna a lokacin
da za shi kogi, ka ce masa, 'Ga abin da UBANGIJI yana cewa, bari mutanena su tafi,
don su yi mini sujada. 21 In ba ka bar mutanena suka tafi ba, zan turo da tarin ƙuda
a kanka da bayinka, a kan mutanenka da cikin gidajenka. Gidajen Masarawa za su
cika da ƙudaje, har ma da ƙasa inda za su taka.
22 " 'Amma zan keɓe yankin Goshen, inda mutanena suke don kada ƙudaje su taɓa
wurin, domin ka sani cewa Ni, UBANGIJI, ina cikin wannan ƙasa. 23 Zan sa iyaka
tsakanin jama'ata da jama'arka. Gobe ne wannan mu'ujiza za tă auku.' "
24 UBANGIJI kuwa ya yi haka. Tarin ƙuda suka zubo a fadar Fir'auna da cikin gidajen
bayinsa, da ko'ina a Masar, ƙasar kuwa ta lalace saboda ƙudaje.
25 Sai Fir'auna ya kira Musa da Haruna ya ce, "Ku tafi, ku miƙa hadaya ga Allahnku,
a nan a cikin ƙasar."
26 Amma Musa ya ce, "Wannan ba zai yiwu ba. Hadayun da mukan miƙa wa
UBANGIJI, Allahnmu haram ne ga Masarawa. In kuwa muka miƙa hadayun da suke
haram a idanunsu, ba za su jajjefe mu ba? 27 Dole mu yi tafiya kwana uku cikin
hamada domin miƙa hadayu ga UBANGIJI Allahnmu, yadda ya umarce mu."
28 Fir'auna ya ce, "Zan bar ku ku tafi, don ku miƙa hadayu ga UBANGIJI Allahnku, a
cikin hamada, amma ba za ku tafi da nisa ba. Yanzu ku yi mini addu'a."
29 Musa ya amsa, "Da zarar na bar ka, zan yi addu'a ga UBANGIJI, gobe kuwa ƙudaje
za su bar Fir'auna da fadawansa da kuma mutanensa. Sai dai a tabbata Fir'auna bai
sāke yin ruɗi ta wurin ƙin barin mutane su tafi su miƙa hadayu ga UBANGIJI ba."
30 Sa'an nan Musa ya rabu da Fir'auna, ya kuma yi addu'a ga UBANGIJI, 31 UBANGIJI
kuwa ya yi abin da Musa ya roƙa. Kudaje suka rabu da Fir'auna da fadawansa da
kuma mutanensa; ba ƙudan da ya rage. 32 Amma a wannan lokaci ma, Fir'auna ya
taurare zuciyarsa, bai kuma bar mutanen suka tafi ba.

## 9

### *Annoba a kan dabbobi*

1 Sai UBANGIJI ya ce wa Musa, "Ka je wurin Fir'auna ka ce masa, 'Ga abin da UBANGIJI
Allah na Ibraniyawa ya ce, "Ka bar mutanena su tafi, domin su yi mini sujada." 2 In

ka ƙi ka bar su su tafi, kana ta riƙonsu, 3 hannun UBANGIJI zai kawo muguwar annoba
a kan dabbobinka a gona, a kan dawakanka, da jakuna da raƙuma, da kuma a kan
shanunka da tumaki da awaki. 4 Amma UBANGIJI zai raba tsakanin dabbobin Isra'ila
da na Masar, saboda kada wata dabbar Isra'ilawa ta mutu.' "
5 Sai UBANGIJI ya sa lokaci ya ce, "Gobe UBANGIJI zai yi wannan a ƙasar." 6 Kashegari
UBANGIJI ya yi haka. Dukan dabbobin Masarawa suka mutu, amma babu dabba guda
ta Isra'ilawan da ta mutu. 7 Fir'auna ya aiki mutane su bincika, sai suka tarar babu
dabba guda ta Isra'ilawan da ta mutu. Duk da haka zuciyar Fir'auna ta taurare, bai
kuwa bar mutanen su tafi ba.

### *Annobar marurai*

8 Sa'an nan UBANGIJI ya ce wa Musa da Haruna, "Dibi tokar matoya cike da tafin
hannuwanku, Musa kuwa zai watsa tokar sama a gaban Fir'auna. 9 Za tă zama ƙura
bisa dukan ƙasar Masar, sai marurai masu zafi su fiffito bisa mutane da dabbobi a
dukan ƙasar."
10 Sai suka ɗibi tokar matoya, suka tsaya a gaban Fir'auna, Musa ya watsa ta a
iska, sai marurai masu zafi suka fiffito bisa mutane da dabbobi. 11 Bokaye suka kāsa
tsayawa a gaban Musa saboda maruran da suke bisansu da a kan dukan Masarawa.
12 Amma UBANGIJI ya taurare zuciyar Fir'auna, bai kuwa saurare Musa da Haruna ba
kamar yadda UBANGIJI ya riga ya ce wa Musa.

### *Annobar ƙanƙara*

13 Sa'an nan UBANGIJI ya ce wa Musa, "Tashi da sassafe, ka sadu da Fir'auna, ka ce
masa, 'Ga abin da UBANGIJI, Allah na Ibraniyawa ya ce, Ka bar mutanena su tafi don
su yi mini sujada, 14 ko kuwa a wannan lokaci zan aika da cikakkiyar annoba mai
ƙarfi a kanka da a kan fadawanka da mutanenka, domin ka san cewa ba kama da ni
a dukan duniya. 15 Gama da ni kaina na miƙa hannuna na buge ka da jama'arka da
annoba, ai, da an hallaka ku a duniya ƙaƙaf. 16 Amma na bar ka ka rayu domin in
nuna maka ikona, domin kuma sunana yă zama abin darajantawa a dukan duniya.
17 Har yanzu kana gāba da mutanena, ba ka kuma bar su su tafi ba. 18 Saboda haka,
gobe war haka, zan sa a yi ƙanƙara mai tsananin gaske, irin wadda Masar ba tă
taɓa gani ba tun kahuwarta, har yă zuwa yanzu. 19 Yanzu, ka ba da umarni a dawo
da shanunku da kuma kome da kuke da shi wanda yake a gona zuwa gida, gama
ƙanƙarar za tă kashe kowane mutum ko dabba wadda take a gona wadda ba a kawo
cikin gida ba, sa'ad da ta fāɗo.' "
20 Waɗansu daga cikin dattawan Fir'auna suka cika da tsoro saboda abin da
UBANGIJI ya faɗa, nan da nan suka shigo da dabbobinsu da bayinsu da sauri daga
gona zuwa cikin gida. 21 Amma waɗanda ba su kula da maganar UBANGIJI ba, suka
bar bayinsu da dabbobi a gona.
22 Sa'an nan UBANGIJI ya ce wa Musa, "Miƙa hannunka sama don a yi ƙanƙara
a bisa dukan Masar, a bisa mutane da dabbobi, da bisa dukan abubuwan da suke
girma a gonakin Masar." 23 Da Musa ya miƙa sandansa sama, sai UBANGIJI ya aiko
da tsawa da ƙanƙara, da walƙiya har ƙasa. Ta haka UBANGIJI ya yi ruwan ƙanƙara
a bisa ƙasar Masar; 24 ƙanƙara ta fāɗo, walƙiya kuma tana ta wulƙawa. Wannan
ce ƙanƙara mafi munin da aka taɓa yi, a dukan ƙasar Masar, tun tarihin kahuwarta
na zaman al'umma. 25 Ko'ina a Masar ƙanƙara ta bugi duk abin da yake a gonaki,
mutane da dabbobi, ta bugi duk ganyaye da suke a gonaki, ta kuma ragargaza kowane
itace. 26 Wuri guda kaɗai da ba a yi ruwan ƙanƙara ba, shi ne yankin Goshen, inda
Isra'ilawa suke.
27 Sai Fir'auna ya aika a kira Musa da Haruna. Ya ce musu, "A wannan karo na
yi zunubi. UBANGIJI, shi ne da gaskiya, ni da mutane mu ke da kuskure. 28 Ku roƙi

UBANGIJI, yǎ tsai da tsawar da ƙanƙarar. Ni kuwa na yi alkawari zan bar ku ku tafi,
ba za ku ƙara tsayawa a nan ba.”
29 Musa ya amsa, “To, da kyau, da zarar na fita daga birnin, zan yi addu’a ga
UBANGIJI, tsawar za tǎ tsaya, ƙanƙarar kuma za tǎ daina, don ku sani cewa duniya
ta UBANGIJI ce. 30 Amma na san cewa kai da fadawanka, har wa yau ba ku ji tsoron
UBANGIJI Allah ba tukuna.”
31 (Rama da sha’ir suka lalace, gama sha’ir ya riga ya nuna, rama kuwa tana fid
da kai. 32 Alkama da gero kam, ba a hallaka su ba, gama lokacin nunansu bai yi ba
tukuna.)
33 Sai Musa ya tashi daga gaban Fir’auna, ya fita daga birni. Da ya miƙa
hannuwansa ta wajen UBANGIJI, sai tsawa da ƙanƙara suka tsaya, kwararowar ruwa
kuma ta ɗauke. 34 Da Fir’auna ya ga cewa ruwa da ƙanƙara da tsawa sun daina, sai
ya sāke yin zunubi. Shi da fadawansa, suka taurare zukatansu. 35 Ta haka zuciyar
Fir’auna ta taurare, bai kuwa bar Isra’ilawa suka tafi ba, kamar yadda UBANGIJI ya
riga ya faɗa ta wurin Musa.

# 10

*Annobar fāra*

1 Sai UBANGIJI ya ce wa Musa, “Je wurin Fir’auna, gama na riga na taurare zuciyarsa
da kuma zukatan fadawansa domin in aikata waɗannan mu’ujizai nawa a tsakiyarsu,
2 don kuma ku gaya wa ’ya’yanku da jikokinku yadda na tsananta wa Masarawa, da
kuma yadda na aikata mu’ujizai a cikinsu, don ku sani ni ne UBANGIJI.”
3 Sai Musa da Haruna suka tafi wurin Fir’auna suka ce masa, “Ga abin da UBANGIJI,
Allah na Ibraniyawa ya ce, ‘Har yaushe za ka ƙi ƙasƙantar da kanka a gabana? Ka
bar mutanena su tafi domin su yi mini sujada. 4 In ka ƙi ka bari su tafi, gobe zan aiko
da fāra a ƙasarka. 5 Za su rufe fuskar ƙasar, har da ba za a iya ganin ƙasa ba. Za
su cinye ɗan sauran abin da ya rage muku daga ɓarnar ƙanƙara, za su cinye dukan
itatuwan da suke girma a gonakinku. 6 Za su cika gidajenka, da na fadawanka, da
na dukan Masarawa, abin da iyayenka da kakanninka ba su taɓa gani ba, tun daga
ranar da suka sami kansu a duniya, har yǎ zuwa yau.’ ” Sa’an nan Musa ya juya, ya
rabu da Fir’auna.
7 Fadawan Fir’auna suka ce masa, “Har yaushe mutumin nan zai zama mana tarko?
Ka bar mutanen su tafi domin su yi wa UBANGIJI Allahnsu sujada. Har yanzu ba ka
san cewa Masar ta lalace ba?”
8 Sa’an nan aka dawo da Musa da Haruna wurin Fir’auna. Sai ya ce, “Ku tafi, ku
yi wa UBANGIJI Allahnku sujada. Amma wa da wa za su tafi?”
9 Musa ya amsa, “Za mu tafi tare da ƙananmu, da tsofaffinmu, da ’ya’yanmu
maza da mata, da kuma garkunanmu na shanu da tumaki, gama dole ne mu yi bikin
ga UBANGIJI.”
10 Fir’auna ya ce, “UBANGIJI ya taimaka bisa ga niyyarku, amma matanku da
ƙananku ba za su tafi ba! A fili yake kuna da niyyar mugunta. 11 Sam! Wannan
ba zai taɓa yiwu ba, sai ko maza kaɗai su tafi su yi wa UBANGIJI sujada, gama abin
da kuke so ke nan.” Sa’an nan aka kori Musa da Haruna daga gaban Fir’auna.
12 Sai UBANGIJI ya ce wa Musa, “Miƙa hannunka a bisa Masar domin fāra su sauko
bisa ƙasar, su ci duk abin da yake girma a gonaki, duk abin da ƙanƙara ta rage.”
13 Saboda haka Musa ya miƙa sandansa bisa Masar, UBANGIJI kuwa ya sa iskar gabas
ta hura a kan ƙasar dukan dare da kuma dukan yini. Da safe kuwa iskar ta kawo fāra;
14 suka mamaye ƙasar duka, suka sauka a ko’ina a ƙasar. Ba a taɓa ganin annobar
fāra haka ba, ba kuwa za a ƙara ganin fāra kamar haka ba. 15 Suka rufe ƙasar har
ta zama baƙi. Suka cinye abin da ƙanƙara ta rage, kowane tsiron da yake girma a

gonaki, da dukan ʼyaʼyan itatuwa. Babu ɗanyen abin da ya ragu a kan itatuwa ko
tsire-tsire a dukan ƙasar Masar.
16 Firʼauna ya kira Musa da Haruna da gaggawa ya ce, "Na yi wa UBANGIJI Allahnku
zunubi, na kuma yi muku. 17 Yanzu ku gafarta mini zunubina a wannan karo, ku
kuma yi adduʼa ga UBANGIJI Allahnku yă ɗauke wannan muguwar annoba daga gare
ni."
18 Sai Musa ya bar Firʼauna ya kuma yi adduʼa ga UBANGIJI. 19 Sai UBANGIJI ya canja
iska zuwa iska mai ƙarfi ta yamma wadda ta ɗibi fārar zuwa Jan Teku. Babu fāran
da suka rage a wani wuri a Masar. 20 Amma UBANGIJI ya taurare zuciyar Firʼauna,
bai kuwa bar Israʼilawa suka tafi ba.

*Annobar duhu*

21 Saʼan nan UBANGIJI ya ce wa Musa, "Miƙa hannunka sama domin a yi duhu a
bisa Masar, duhun da za a iya taɓawa." 22 Sai Musa ya miƙa hannunsa sama, aka
kuma yi duhu baƙi ƙirin bisa dukan ƙasar Masar na kwana uku. 23 Ba wanda ya iya
gani wani ko yă bar wurinsa na kwana uku. Amma dukan Israʼilawa sun kasance da
haske a inda suke zama.
24 Sai Firʼauna ya aika aka kira Musa, ya kuma ce, "Ku tafi, ku yi wa UBANGIJI sujada.
Matanku da yaranku ma za su iya tafiya tare da ku; sai dai ku bar garkunanku na
shanu da tumaki."
25 Amma Musa ya ce, "Dole ka bari mu kasance da hadayu, da kuma hadayu na
ƙonawa waɗanda za mu miƙa wa UBANGIJI Allahnmu. 26 Dole dabbobinmu ma su
tafi tare da mu; ko kofato ma, ba za a bari a baya ba. A cikinsu ne za mu ɗibi abin
da za mu yi wa UBANGIJI Allahnmu sujada. Ba mu kuma san irin abin da za mu miƙa
wa UBANGIJI ba, sai mun kai can."
27 Amma UBANGIJI ya taurare zuciyar Firʼauna, har bai yarda yă sake su ba.
28 Firʼauna ya ce wa Musa, "Fita, ka ba ni wuri! Ka mai da hankali, kada ka ƙara
bayyana a gabana, gama ran da ka sāke ganin fuskata, a ran nan za ka mutu."
29 Musa ya amsa, "Madalla, kamar yadda ka faɗa, ba zan ƙara bayyana a gabanka
ba."

# 11

*Annoba a kan ɗan fari*

1 To, fa, sai UBANGIJI ya ce wa Musa, "Zan ƙara kawo annoba guda a kan Firʼauna
da kan Masar. Bayan haka, zai bar ku, ku fita daga nan. Saʼad da ya yi haka kuwa,
zai kore ku gaba ɗaya. 2 Ka faɗa wa mutane cewa dukan maza da mata, su roƙi
maƙwabtansu kayan azurfa da na zinariya." 3 (UBANGIJI ya sa mutane suka sami
tagomashi a idon Masarawa, Musa kuwa ya sami girma sosai a cikin ƙasar Masar a
gaban fadawan Firʼauna da kuma a gaban jamaʼar.)
4 Saboda haka Musa ya ce, "Ga abin da UBANGIJI ya ce, ʻWajen tsakar dare, zan
ratsa dukan Masar. 5 Kowane ɗan fari, namiji, a Masar zai mutu, daga kan ɗan fari
na Firʼauna wanda zai ci gadon sarauta, har zuwa kan ɗan fari na baiwa, wadda take
niƙa, da kuma dukan ʼyan farin shanu. 6 Za a yi kuka mai zafi koʼina a Masar, irin
wadda ba a taɓa yi ba, ba kuwa za a ƙara yi ba. 7 Amma a cikin Israʼilawa, ba karen
da zai yi haushi wa mutum ko dabba.ʼ Ta haka za ku sani UBANGIJI zai bambanta
tsakanin Masar da Israʼila. 8 Dukan fadawan nan naka za su zo wurina, suna fāɗi a
gabana suna cewa, ʻKa fita, kai da dukan jamaʼarka!ʼ Saʼan nan zan fita." Daga nan
sai Musa ya fita daga gaban Firʼauna a husace.
9 UBANGIJI ya ce wa Musa, "Firʼauna zai ƙi kasa kunne gare ka, sai na ƙara aikata
waɗansu muʼujizai cikin Masar." 10 Musa da Haruna suka aikata dukan waɗannan

mu'ujizai a gaban Fir'auna, amma UBANGIJI ya taurare zuciyar Fir'auna, bai kuwa bar Isra'ilawa su fita daga ƙasarsa ba.

# 12

*Bikin Ketarewa*

1 UBANGIJI ya ce wa Musa da Haruna a Masar, 2 "Wannan wata za tă zama a gare ku
wata na farko, wata na fari na shekararku. 3 Ka faɗa wa dukan jama'ar Isra'ila cewa
a rana ta goma ga wannan wata, kowane mutum zai ɗauki ɗan rago domin iyalinsa,
ɗaya domin kowane gida. 4 In akwai wani gidan da ba za su iya cinye rago guda
ɗungum ba, saboda iyalin kima ne, to, sai su haɗa kai da maƙwabtansu, su ɗauki
rago guda gwargwadon yawansu, bisa ga abin da mutum guda zai ci. 5 Dabbobin
da za ku zaɓa, dole su zama bana ɗaya, namiji marar tabo, za ku kuma kamo su
daga cikin tumaki ko awaki. 6 Za ku turke dabbar har rana ta goma sha huɗu ga
wata, wato, sa'ad da dukan taron jama'ar Isra'ila za su yanka ragunansu da yamma.
7 Sa'an nan za su ɗauki jinin, su shafa a gefen da yake saman dogaran ƙofa na gidajen
da suke cin naman dabbobin. 8 A wannan dare, za su gasa naman, su ci da ganyaye
masu ɗaci, da kuma burodi marar yisti. 9 Kada ku ci nama ɗanye, ko kuma dafaffe,
amma a gasa shi, da kan, da ƙafafun, da kuma kayan cikin. 10 Kada ku bar kome yă
kai gobe, abin da ya kai gobe kuwa, sai ku ƙone shi. 11 Ga yadda za ku ci shi, ku yi
ɗamara, takalma kuwa a ƙafafunku, kuna riƙe da sandunan tafiya a hannunku. Ku
ci shi da gaggawa; Bikin Ketarewa ne na UBANGIJI.
12 "A wannan dare, zan ratsa Masar, in bugi kowane ɗan fari, na mutum da na
dabba, zan kuma hukunta dukan gumakan Masar. Ni ne UBANGIJI. 13 Jinin zai zama
alama a gare ku, a gidajen da kuke; sa'ad da kuwa na ga jinin, zan ƙetare ku. Ba
wata annoba mai hallakarwa da za tă taɓa ku yayinda na bugi Masar.
14 "Wannan rana za tă zama muku abin tunawa dukan zamananku masu zuwa, za
ku kiyaye ta kamar biki ga UBANGIJI, dawwammamiyar farilla ce har abada. 15 Kwana
bakwai za ku ci burodi marar yisti. A rana ta fari, za ku fid da yisti daga gidajenku
gama duk wanda ya ci abu mai yisti daga rana ta fari har zuwa rana ta bakwai, za
a fid da shi daga Isra'ila. 16 A rana ta fari, za ku yi taro mai tsarki, haka kuma za
ku sāke yi a rana ta bakwai. Kada ku yi aiki a waɗannan ranaku, sai dai ku shirya
abinci domin kowa, abin da za ku yi ke nan kawai.
17 "Ku yi Bikin Burodi Marar Yisti domin a wannan rana ce na fitar da ku ɓangare-
ɓangare daga Masar. Ku kiyaye wannan rana ta zama muku dawwammamiyar farilla
wa tsara masu zuwa. 18 A wata na fari, za ku ci burodi marar yisti daga yammancin
ranar goma sha huɗu har zuwa yammancin ranar ashirin da ɗaya. 19 Kada a sami
yisti a gidajenku har kwana bakwai. Kuma duk wanda ya ci wani abu mai yisti, za a
fid da shi daga taron jama'ar Isra'ila, ko baƙo ne, ko haifaffen ɗan ƙasa. 20 Kada ku
ci wani abincin da aka yi da yisti. Ko'ina kuka zauna, dole ku ci burodi marar yisti."
21 Sa'an nan Musa ya kira dukan dattawan Isra'ila ya ce musu, "Ku je da sauri ku
zaɓi dabbobin iyalanku, ku yanka ragon Bikin Ketarewa. 22 Ku ɗauki ƙunshin itacen
hizzob, ku tsoma cikin jinin da yake a kwano, ku yayyafa wa dogaran ƙofa duka biyu,
da bisa kan ƙofar. Kada wani daga cikinku yă fita daga ƙofar gidansa sai da safe.
23 Sa'ad da UBANGIJI yake ratsa ƙasar don yă bugi Masarawa, zai ga jinin a bisa da
kuma gefen madogaran ƙofa, zai ƙetare ƙofar, ba zai bar mai hallakawa yă shiga
gidajenku, yă buge ku ba.
24 "Ku kiyaye waɗannan dokokin a matsayin dawwammamiyar farilla, da ku da
'ya'yanku har abada. 25 Sa'ad da kuka shiga ƙasar da UBANGIJI zai ba ku yadda
ya alkawarta, ku kiyaye wannan biki. 26 Sa'ad da kuma 'ya'yanku suka tambaye
ku, 'Mece ce manufar wannan biki?' 27 Sai ku faɗa musu, 'Hadaya ce ta Bikin

Ketarewa ga UBANGIJI, domin ya tsallake gidajen Isra'ilawa a Masar, lokacin da ya
kashe Masarawa, amma bai taɓa gidajenmu ba.' " Sai mutane suka rusuna, suka yi
sujada. 28 Isra'ilawa suka tafi suka yi yadda UBANGIJI ya umarci Musa da Haruna.
29 Da tsakar dare, sai UBANGIJI ya karkashe dukan 'ya'yan fari a ƙasar Masar, tun
daga ɗan farin Fir'auna, wato, magājinsa, har zuwa ɗan fari na ɗan sarƙa da yake
kurkuku, har da 'ya'yan fari na dabbobi. 30 Fir'auna da dukan fadawansa da kuma
dukan Masarawa, suka tashi a cikin daren da kuka mai zafi, aka kuma ji kukan a
ko'ina a cikin ƙasar Masar, gama ba gidan da ba a yi mutuwa ba.

### *Fitowa*

31 A cikin daren, Fir'auna ya aika a kira Musa da Haruna ya ce, "Ku tashi, ku da
jama'arku, ku fita daga cikin jama'ata. Ku tafi, ku bauta wa UBANGIJI yadda kuka ce.
32 Ku kwashi garkunanku na tumaki da na awaki, da na shanu, ku yi tafiyarku kamar
yadda kuka ce, amma ku sa mini albarka."
33 Masarawa suka matsa wa Isra'ilawa su fita daga ƙasarsu da sauri. Gama
mutanen Masar sun ce, "Ai, za mu mutu duka, in ba su tafi ba!" 34 Sai mutanen
suka ɗauki garin da sun kwaɓa ba yisti a ciki, tare da ƙwaryansu na aikin kwaɓan,
suka nannaɗe su a mayafansu, suka rataye a kafaɗunsu. 35 Isra'ilawa kuwa suka
yi yadda Musa ya umarce su, suka roƙi Masarawa kayan adonsu na azurfa da na
zinariya, da kuma tufafi. 36 UBANGIJI kuwa ya sa Isra'ilawa suka yi farin jini a wurin
Masarawa, Masarawa kuma suka saki hannu wa mutanen, suka ba su duk abin da
suka roƙa; ta haka Isra'ilawa suka washe Masarawa.
37 Isra'ilawa suka kama tafiya daga Rameses zuwa Sukkot. Akwai maza dubu ɗari
shida da suke tafiya da ƙafa, ban da mata da yara. 38 Waɗansu mutane da yawa da
ba Isra'ilawa ba, suka haura tare da su, da garkunan shanu, da na tumaki da awaki.
39 Suka toya burodi marar yisti da garin da aka kwaɓa wanda suka kawo daga Masar.
Garin da aka kwaɓan ba shi da yisti, domin an kore su daga Masar, ba su kuwa sami
damar shirya wa kansu abinci ba.
40 Zaman da Isra'ilawa suka yi a Masar, ya kai shekara 430. 41 A ranar da shekara
430 ɗin nan suka cika, a ran nan ne dukan ɓangare-ɓangare na mutanen UBANGIJI
suka bar Masar. 42 Gama UBANGIJI ya yi tsaro a wannan dare, domin yă fitar da
su daga Masar, a wannan dare, dole dukan Isra'ilawa su yi tsaro, don su girmama
UBANGIJI, cikin dukan tsararraki masu zuwa.

### *Abubuwan da Bikin Ketarewa ya hana*

43 UBANGIJI ya ce wa Musa da Haruna, "Waɗannan ne ƙa'idodin Bikin Ketarewa.
"Ba baƙon da zai ci shi. 44 Duk bawan da kuka sayo, yana iya ci, in dai an yi masa
kaciya, 45 amma wanda ba ya zama tare da ku na ɗinɗinɗin, da kuma wanda aka
ɗauki hayansa, ba zai ci ba.
46 "Dole a ci shi a cikin gida ɗaya; kada a kai naman waje. Kada a karya wani daga
ƙasusuwansa. 47 Dole dukan taron jama'ar Isra'ila su yi bikin.
48 "Baƙon da yake zama tare da ku da yake so yă yi Bikin Ketarewar UBANGIJI,
dole yă yi wa dukan mazan da suke cikin gidansa kaciya; sa'an nan ne zai iya yin
abubuwa kamar haifaffen ɗan ƙasa. 49 Wannan za tă zama dawwammamiyar farilla
ta shafi ɗan ƙasa da kuma baƙon da yake zama a tsakaninku."
50 Dukan Isra'ilawa suka yi na'am da shi, suka yi yadda UBANGIJI ya umarci Musa
da Haruna. 51 A wannan rana, UBANGIJI ya fito da Isra'ilawa ɓangare-ɓangare daga
Masar.

# 13

### *Keɓewar ɗan fari*

1 UBANGIJI ya ce wa Musa, 2 "Keɓe mini kowane ɗan fari. Ɗan fari wanda ya fara
buɗe mahaifa a cikin Isra'ilawa nawa ne, ko na mutum ko na dabba."
3 Sai Musa ya ce wa mutane, "Ku tuna da wannan rana, ranar da kuka fito daga
Masar, daga ƙasar bauta, gama UBANGIJI ya fito da ku da hannu mai iko. Kada ku ci
wani abin da yake da yisti. 4 A wannan rana kuka fita, wato, a watan Abib. 5 Sa'ad
da UBANGIJI ya kawo ku cikin ƙasar Kan'aniyawa, Hittiyawa, Amoriyawa, Hiwiyawa
da Yebusiyawa, ƙasar da ya rantse wa kakanninku cewa zai ba ku, ƙasar da take zub
da madara da zuma, za ku kiyaye wannan biki a wannan wata. 6 Kwana bakwai za
ku ci burodi marar yisti, a kan rana ta bakwai kuma za ku yi biki ga UBANGIJI. 7 Ku
ci burodi marar yisti cikin kwana bakwai; kada a sami wani abu mai yisti a cikinku,
ko a sami yisti a ko'ina a wurinku. 8 A ranan nan kowa zai faɗa wa ɗanka, 'Ina yin
haka saboda abin da UBANGIJI ya yi mini, sa'ad da na fita daga Masar.' 9 Wannan abin
tunawa zai zama muku alama a hannunku, da kuma a goshinku cewa dokar UBANGIJI
tana a bakinku. Gama UBANGIJI ya fitar da ku daga Masar da hannu mai iko. 10 Dole
ku kiyaye wannan farilla kowace shekara a lokacinta.
11 "Bayan UBANGIJI ya kawo ku cikin ƙasar Kan'aniyawa, ya kuma ba da ita yadda
ya alkawarta muku da rantsuwa, ku da kakanninku, 12 sai ku miƙa kowane ɗan fari
ga UBANGIJI. Duk ɗan farin dabbobinku na UBANGIJI ne. 13 Amma a fanshi kowane
ɗan farin jakinku da ɗan rago. In kuwa ba za ku fanshe shi ba, sai ku karye wuyansa.
Sai ku fanshe kowane ɗan farin daga cikin 'ya'yanku.
14 "A kwanaki masu zuwa, in ɗanka ya tambaye ka, 'Mene ne manufar wannan?'
Ka faɗa masa cewa, 'Da hannu mai iko UBANGIJI ya fito da mu daga Masar, daga
ƙasar bauta. 15 Sa'ad da Fir'auna ya taurare zuciyarsa, bai yarda ya sallame mu ba,
sai UBANGIJI ya kashe dukan 'ya'yan farin ƙasar Masar, na mutum da na dabba, gaba
ɗaya. Domin haka nake yin hadaya ga UBANGIJI da 'ya'yan fari, maza, da suka fara
buɗe mahaifa, amma nakan fanshi dukan 'ya'yan farina maza.' 16 Za tă kuma zama
alama a hannunku da kuma shaida a goshinku cewa UBANGIJI ya fito da mu daga
Masar da hannunsa mai iko."

### *Ketarewar teku*

17 Sa'ad da Fir'auna ya bar mutane su tafi, Allah bai bi da su a hanyar da ta bi
ta iyakar Filistiyawa ba, ko da yake wannan hanya ce ta fi kusa. Gama Allah ya ce,
"In suka fuskanci yaƙi, wataƙila su canja ra'ayinsu su koma Masar." 18 Saboda haka
Allah ya kewaye da mutanen ta hamada zuwa Jan Teku. Isra'ilawa kuwa suka fita
daga Masar da shirin yaƙi.
19 Musa ya ɗauki ƙasusuwan Yusuf tare da shi, gama Yusuf ya sa Isra'ilawa su
rantse masa. Ya ce, "Tabbatacce Allah zai taimake ku, sai ku ɗibi ƙasusuwana tare
da ku daga wannan wuri."*
20 Bayan sun bar Sukkot sai suka kafa sansani a Etam a bakin hamada. 21 Da
rana UBANGIJI yakan ja gabansu a cikin al'amudin girgije domin yă bishe su a kan
hanyarsu, da dare kuma a cikin al'amudin wuta domin yă ba su haske, domin su iya
tafiya dare da rana. 22 Al'amudan nan biyu, na girgije da na wuta, ba su daina yi wa
jama'a jagora ba.

## 14

1 Sa'an nan UBANGIJI ya ce wa Musa, 2 "Ka faɗa wa Isra'ilawa, su juya su kafa
sansani a Fi Hahirot, a tsakanin Migdol da teku. Za su kafa sansanin kai tsaye kusa da
teku, wanda ya fuskanci Ba'al-Zafon. 3 Fir'auna zai yi tsammani, 'Aha, Isra'ilawa sun
rikice cikin ƙasar, hamada kuwa ta yimƙe su.' 4 Zan kuma taurare zuciyar Fir'auna,
zai kuwa bi su. Na shirya wannan domin in nuna ɗaukakata a bisa Fir'auna da

* **13:19** Dubi Far 50.25.

ƙungiyar sojansa. Bayan wannan, mutanen Masar za su sani ni ne UBANGIJI.” Sai
Isra’ilawa suka yi haka.

5 Sa’ad da aka faɗa wa Fir’auna cewa Isra’ilawa sun gudu, sai Fir’auna da bayinsa
suka canja ra’ayinsu game da su, suka ce, “Me muka yi? Mun bar Isra’ilawa suka
tafi, mun kuwa rasa hidimarsu!” 6 Sai shi da keken yaƙinsa suka shirya, ya kuma
ɗauki sojojinsa tare da shi. 7 Ya ɗauki kekunan yaƙi ɗari shida mafi kyau duka, tare
da duk sauran keken yaƙin Masar, da shugabanni kuma a kan dukansu. 8 UBANGIJI ya
taurare zuciyar Fir’auna sarkin Masar, domin yǎ bi Isra’ilawa waɗanda suke tafiya
ba tsoro. 9 Masarawa, dukan dawakan Fir’auna da kekunan yaƙi da mahaya da sojoji,
suka bi Isra’ilawa suka cin musu yayinda suke a sansani kusa da teku kurkusa da Fi
Hahirot, wanda ya fuskanci Ba’al-Zafon.

10 Da Fir’auna ya yi kusa, Isra’ilawa suka ɗaga idanu sai suka hange Masarawa
daga nesa suna tā da ƙura suna zuwa. Sai suka tsorata ƙwarai, suka kuwa yi kuka
ga UBANGIJI. 11 Suka ce wa Musa, “Don babu makabarta a Masar ne, ka kawo mu a
hamada mu mutu? Me ka yi mana ke nan da ka fitar da mu daga Masar? 12 Ba mu
faɗa maka a Masar ba, cewa ‘Ka bar mu mu bauta wa Masarawa’? Ai, da ya fi mana
mu bauta wa Masarawa, da a ce mu mutu a hamada!”

13 Musa ya amsa wa mutane ya ce, “Kada ku ji tsoro. Ku tsaya dai ku ga ceton da
UBANGIJI zai kawo muku yau. Masarawan da kuke gani yau, ba za ku ƙara ganinsu
ba. 14 UBANGIJI zai yi yaƙi dominku, ku dai tsaya kurum.”

15 Sa’an nan UBANGIJI ya ce wa Musa, “Don me kake mini kuka? Ka faɗa wa
Isra’ilawa su ci gaba da tafiya. 16 Ka ɗaga sandanka, ka miƙa shi bisa teku don
ruwa yǎ rabu domin Isra’ilawa su wuce cikin teku a kan busasshiyar ƙasa. 17 Zan
taurare zukatan Masarawa su shiga don su bi su. Ta haka zan ci nasara bisa Fir’auna
da rundunansa, da keken yaƙinsa, da mahayan dawakansa. 18 Masarawa za su sani
ni ne UBANGIJI sa’ad da na sami nasara bisa kan Fir’auna, da keken yaƙinsa, da
mahayan dawakansa.”

19 Sai mala’ikan Allah wanda yake tafiya a gaban sojojin Isra’ila, ya janye, ya koma
bayansu. Al’amudin girgije shi ma ya koma, ya tsaya a bayansu, 20 ya dawo tsakanin
sojojin Masar da na Isra’ila. Duk dare, girgijen ya jawo duhu ga gefe ɗaya, haske
kuma ga ɗaya gefen; saboda haka ba wanda ya kusaci wani duk dare.

21 Da Musa ya miƙa hannunsa a bisa teku, sai UBANGIJI ya tura teku baya da
iskar gabas mai ƙarfi duk dare, ya maishe shi busasshiyar ƙasa. Ruwa ya rabu,
22 sai Isra’ilawa suka wuce cikin teku a kan busasshiyar ƙasa, ruwan ya zama musu
katanga dama da hagu.

23 Masarawa suka bi su da dukan dawakan Fir’auna, da kekunan yaƙi, da mahayan,
suka bi su cikin teku. 24 Da asubahin fāri, sai UBANGIJI ya dubi ƙasa a kan sojojin
Masarawa daga al’amudin wuta da kuma girgije, sai ya sa suka ruɗe. 25 Ya sa ƙafafun
keken yaƙinsu suka fita don su kāsa tuƙi. Sai Masarawa suka ce, “Bari mu gudu daga
Isra’ilawa gama UBANGIJI yana yaƙi dominsu gāba da Masar.”

26 Sa’an nan UBANGIJI ya ce wa Musa, “Miƙa hannunka bisa teku don ruwa yǎ koma
kan Masarawa, da keken yaƙinsu, da kuma mahayansu.” 27 Musa ya miƙa hannunsa
a bisa tekun, da wayewar gari kuwa teku ya koma wurinsa na dā. Masarawa suka yi
ƙoƙari su gudu, sai UBANGIJI ya tura su cikin teku. 28 Ruwan ya komo ya rufe keken
yaƙin da mahayan, dukan sojojin Fir’aunan da suka bi bayan Isra’ilawa cikin teku,
ba ko ɗaya da ya tsira.

29 Amma Isra’ilawa suka wuce cikin teku a busasshiyar ƙasa, ruwa kuwa ya yi
musu katanga dama da hagu. 30 A rana nan UBANGIJI ya cece Isra’ila daga hannuwan
Masarawa, Isra’ilawa kuwa suka ga gawawwakin Masarawa a bakin teku. 31 Sa’ad da

Isra'ilawa suka ga iko mai girma da UBANGIJI ya yi gāba da Masarawa, sai mutanen
suka ji tsoron UBANGIJI, suka amince da shi, da kuma bawansa Musa.

# 15

*Waƙar Musa da Miriyam*

1 Sa'an nan Musa da Isra'ilawa suka rera wannan waƙa ga UBANGIJI suka ce,
"Zan rera waƙa ga UBANGIJI
gama an ɗaukaka shi ƙwarai.
Doki da mahayinsa
ya jefa su cikin teku.

2 "UBANGIJI ne ƙarfina da mafakata,
ya zama cetona.
Shi Allahna ne, zan yabe shi.
Allah na kakana, zan ɗaukaka shi.
3 UBANGIJI mai yaƙi ne
UBANGIJI ne sunansa.
4 Karusan Fir'auna da sojojinsa
ya jefa cikin teku.
Zaɓaɓɓun jarumawansa ya nutsar da su cikin Bahar Maliya.
5 Zurfafan ruwaye sun rufe su;
suka nutse cikin zurfi kamar dutse.
6 Hannun damanka, ya UBANGIJI,
Mai kwarjini ne da iko,
hannun damanka, ya UBANGIJI,
ya farfashe magabci.

7 "A cikin girman kwarjininka
ka kā da waɗanda sun yi gāba da kai.
Ka aiki fushinka mai zafi
ya cinye su kamar tattaka.
8 Da hucin numfashin hancinka
ruwaye suka tattaru.
Ruwaye masu kwararowa, suka tsaya kamar bango;
ruwaye na zurfafa suka daskare a tsakiyar teku.
9 Magabci ya yi fahariya, cewa
'Zan fafare su, in ci musu.
Zan raba ganima;
abin da na so ya samu.
Zan ja takobina
hannuna kuwa zai hallaka su.'
10 Amma ka hura numfashinka
sai teku ya rufe su.
Suka nutse kamar darma
cikin manyan ruwaye.
11 Wane ne cikin alloli,
ya yi kamar ka, ya UBANGIJI?
Wane ne kamar ka,
mai ɗaukaka cikin tsarki,
mai banrazana cikin ɗaukaka,
mai aikata al'ajabai?

12 “Ka miƙa hannunka na dama,
ƙasa ta haɗiye abokan gābanka.
13 A cikin ƙaunarka marar iyaka, za ka bishe
mutanen da ka fansa.
A cikin ƙarfinka, za ka bishe su
zuwa mazauninka mai tsarki.
14 Al’ummai za su ji, su yi rawar jiki
tsoro zai kama mutanen Filistiya.
15 Sarakunan Edom za su tsorata,
shugabannin Mowab za su yi rawar jiki,
mutanen Kan’ana za su narke.
16 Razana da tsoro za su fāɗo a kansu.
Da ikon hannunka
za su tsaya cik kamar dutse,
har sai mutanen da ka kawo sun wuce, ya UBANGIJI.
17 Za ka kawo su, ka dasa su
a kan dutsen nan naka
inda, ya UBANGIJI, ka shirya domin mazauninka,
wuri mai tsarkin da hannuwanka suka kafa, ya UBANGIJI.

18 “UBANGIJI zai yi mulki
har abada abadin.”
19 Sa’ad da dawakai, kekunan yaƙi da mahayan dawakan Fir’auna suka shiga cikin
teku, UBANGIJI ya mayar da ruwan teku a kansu, amma Isra’ilawa suka wuce a cikin
teku a busasshiyar ƙasa. 20 Sa’an nan Miriyam annabiya, ’yar’uwar Haruna ta ɗauki
ganga a hannunta, dukan mata kuwa suka bi ta, da ganguna suna rawa. 21 Miriyam
ta yi musu waƙa.
“Ku rera ga UBANGIJI
gama ya ci gawurtacciyar nasara.
Doki da mahayi,
ya jefa cikin teku.”

*Ruwayen Mara da Elim*

22 Sai Musa ya jagoranci Isra’ila daga jan teku zuwa hamadar Shur. Kwana uku
suka yi tafiya cikin hamada ba su sami ruwa ba. 23 Da suka zo Mara, ba su iya shan
ruwan ba saboda yana da ɗaci (shi ya sa ake kira wurin Mara). 24 Sai mutanen suka
yi gunaguni a kan Musa, suna cewa, “Me za mu sha?”
25 Sai Musa ya yi kuka ga UBANGIJI, UBANGIJI kuwa ya nuna masa wani itace. Sai ya
jefa shi cikin ruwan, sai ruwan ya zama mai daɗi.
A can UBANGIJI ya yi musu doka da farilla, a can kuma ya gwada su. 26 Ya ce, “In kun
kasa kunne ga muryar UBANGIJI Allahnku kuka yi abin da yake daidai a idanunsa, in
kun mai da hankali ga umarnansa, kuka kiyaye dukan farillansa, ba zan kawo muku
wani ciwon da na kawo a kan Masarawa ba, gama ni ne UBANGIJI da nake warkar da
ku.”
27 Sai suka zo Elim inda akwai maɓulɓulan ruwa goma sha biyu da itatuwan dabino
saba’in, suka sauka a can, kusa da ruwa.

# 16

*Manna da makware*

1 Dukan taron Isra’ila suka tashi daga Elim suka zo hamadar Sin, wadda take
tsakanin Elim da Sinai, a rana ta goma sha biyar ga wata biyu, bayan sun fito daga
Masar. 2 A hamadan, dukan taro suka yi gunaguni a kan Musa da Haruna. 3 Isra’ilawa

suka ce musu, “Da ma a hannun UBANGIJI ne muka mutu a Masar, inda muka zauna
kewaye da tukwanen nama, muna cin duk abincin da muke so, amma kun kawo mu
cikin wannan hamada don ku kashe dukan wannan taro da yunwa.”
4 Sai UBANGIJI ya ce wa Musa, “Zan zubo muku burodi kamar ruwa daga sama.
Mutanen za su fita kowace rana su tattara abin da zai ishe su na ranan. Ta haka
zan gwada su in ga ko za su bi umarnaina. 5 A rana ta shida za su shirya abin da
suka kwaso, wannan kuwa zai zama ninki biyu na abin da sukan tattara na sauran
ranaku.”
6 Saboda haka Musa da Haruna suka ce wa dukan Isra’ila, “Da yamma za ku sani
UBANGIJI ne ya fitar da ku daga Masar. 7 Da safe za ku ga ɗaukakar UBANGIJI, saboda
ya ji gunaguninku a kansa. Wane mu, da za ku yi gunaguni a kanmu?” 8 Musa ya
kuma ce, “Za ku san cewa shi ne UBANGIJI, sa’ad da ya ba ku nama ku ci da yamma,
da kuma duk burodin da kuke so da safe, saboda ya ji gunagunin da kuka yi a kansa.
Namu a wane? Ai, gunaguninku ba a kanmu ba, amma a kan UBANGIJI ne.”
9 Sai Musa ya ce wa Haruna, “Ka faɗa wa dukan taron Isra’ila, ‘Ku zo gaban
UBANGIJI, gama ya ji gunaguninku.’ ”
10 Yayinda Haruna yake magana da dukan taron Isra’ila, sai suka duba wajen
hamada, sai ga ɗaukakar UBANGIJI tana bayyana a girgije.
11 UBANGIJI ya ce wa Musa, 12 “Na ji gunagunin Isra’ilawa. Ka faɗa musu, ‘A tsakanin
fāɗuwar rana da almuru, za ku ci nama, da safe kuma za ku ƙoshi da burodi. Sa’an
nan za ku sani ni ne UBANGIJI Allahnku.’ ”
13 Da yamman wannan rana, sai makware suka rufe dukan sansani, da safe kuma
sai ga raɓa ta kewaye sansani. 14 Lokacin da raɓar ta watse, sai ga wani abu kamar
tsaki, falle-falle kuma da laushi, fari, kamar hazo, a ƙasa. 15 Sa’ad da Isra’ilawa suka
ga wannan, sai suka ce wa junansu, “Mene ne wannan?” Gama ba su san ko mene
ne ba.
Musa ya ce musu, “Wannan shi ne burodin da UBANGIJI ya ba ku ku ci. 16 Wannan
shi ne abin da UBANGIJI ya umarta, ‘Kowane mutum zai tattara bisa ga bukatarsa. Ku
tara rabin gallon don mutum guda da yake cikin tentinku.’ ”
17 Isra’ilawa suka yi kamar yadda aka faɗa musu, waɗansu suka tattara da yawa,
waɗansu kuma kaɗan. 18 Da suka gwada a mudu, wanda ya tattara da yawa bai sami
mafi yawa ba, wanda kuma ya tattara kaɗan bai sami ƙanƙani ba. Kowane mutum
ya tattara daidai bukatarsa.
19 Sa’an nan Musa ya ce musu, “Kada wani yă bar saura har safe.”
20 Duk da haka waɗansu ba su kula da umarnin Musa ba, suka bar saura har safe,
kashegari kuwa ta yi tsutsotsi, ta ruɓe, sai Musa ya yi fushi da su.
21 Kowace safiya, kowanne mutum yakan tattara daidai bukatarsa, lokacin da rana
ta yi zafi, sai ta narke. 22 A rana ta shida, suka tattara ninki biyu, mudu biyu ga
mutum guda, sai shugabannin taron suka zo suka kawo ƙara wurin Musa. 23 Shi
kuma ya ce musu, “Wannan shi ne umarnin UBANGIJI, ‘Gobe za tă zama ranar hutu,
Asabbaci mai tsarki ga UBANGIJI. Domin haka sai ku toya abin da kuke so ku toya, ku
kuma dafa abin da kuke so ku dafa. Abin da ya rage ku ajiye har safe.’ ”
24 Sai suka bar saura har safe, kamar yadda Musa ya umarta, bai kuwa yi wari ko
yă yi tsutsa ba. 25 Musa ya ce, “Ku ci shi yau, saboda yau Asabbaci ne na UBANGIJI.
Ba za ku same shi a ƙasa a yau ba. 26 Kwana shida za ku tattara shi, amma a rana ta
bakwai, Asabbaci, ba za a same shi ba.”
27 Duk da haka waɗansu mutane suka fita a ranar Asabbaci don su tattara, amma
ba su sami kome ba. 28 Sai UBANGIJI ya ce wa Musa, “Har yaushe za ku ƙi bin dokokina
da umarnaina? 29 Ku lura fa, ai, UBANGIJI ne ya ba ku Asabbaci; shi ya sa a kan ba
ku burodi na kwana biyu, a rana ta shida. Kowa ya kamata yă kasance inda yake a
rana ta bakwai; kada kowa yă fita.” 30 Sai mutanen suka huta a rana ta bakwai.

31 Mutanen Isra'ila suka kira burodin Manna. Manna yana nan fari kamar farin
riɗi, ɗanɗanonsa kuma yana kama da masa da aka yi da zuma. 32 Musa ya ce,
"Wannan shi ne abin da UBANGIJI ya umarta, 'Ku auna mudu guda na Manna, a
adana ta dukan zamananku, domin kowane zamani yă ga irin abincin da na ba ku
ku ci a hamada, yayinda na fitar da ku daga Masar.' "
33 Saboda haka Musa ya ce wa Haruna, "Ka ɗauki tulu, ka sa mudu guda na Manna
a ciki. Sa'an nan ka sa shi a gaban UBANGIJI, don a adana don tsararraki masu zuwa."
34 Sai Haruna ya ajiye Mannar a gaban Akwatin Alkawari, don a adana ta kamar
yadda UBANGIJI ya umarci Musa. 35 Isra'ilawa suka yi shekaru arba'in suna cin
Manna, har sai da suka shiga cikin ƙasar da take da mutane, suka ci Manna har
zuwa kan iyakar ƙasar Kan'ana.
36 (Omer guda, daidai ne da kashi ɗaya bisa goma na Efa.)

# 17

*Ruwa daga dutse*

1 Dukan taron Isra'ilawa suka kama tafiya daga Hamadar Sin, suka yi ta tafiya
suna sauka a wurare dabam-dabam bisa ga umarnin UBANGIJI. A ƙarshe suka sauka
a Refidim, suka zauna a can, amma ba ruwan da jama'a za su sha. 2 Saboda haka
suka yi wa Musa maganganun banza suka ce, "Ba mu ruwa mu sha."

Musa ya amsa ya ce, "Don me kuke mini maganganun banza? Don me kuke gwada
UBANGIJI?"
3 Amma mutanen suka yi fama da ƙishirwa a can, suka yi gunaguni a kan Musa.
Suka ce, "Don me ka fitar da mu daga Masar, ka sa mu da 'ya'yanmu da dabbobinmu,
mu mutu da ƙishirwa?"
4 Sai Musa ya yi kuka ga UBANGIJI ya ce, "Me zan yi da wannan jama'a? Suna shiri
su jajjefe ni da duwatsu."
5 UBANGIJI amsa wa Musa, "Ka ɗauki sandan da ka bugi ruwan Nilu da shi. Ka
kira waɗansu shugabannin Isra'ila, ku wuce a gaban jama'ar. 6 Zan tsaya a can a
gabanka, kusa da dutsen Horeb. Ka bugi dutsen, ruwa kuwa zai fito daga gare shi
domin mutane su sha." Sai Musa ya yi haka a idon dattawan Isra'ila. 7 Sai suka ba wa
wurin suna, Massa da Meriba, saboda Isra'ilawa sun yi jayayya, suka kuma gwada
UBANGIJI cewa, "UBANGIJI yana tsakaninmu ko babu?"

*An ci Amalekawa da yaƙi*

8 Amalekawa suka zo, suka yaƙi Isra'ilawa a Refidim. 9 Musa ya ce wa Yoshuwa,
"Zaɓi waɗansu mazanmu, ka je ka yaƙi Amalekawa. Gobe zan tsaya a bisa tudu, da
sandan Allah a hannuwana."
10 Sai Yoshuwa ya yaƙi Amalekawa kamar yadda Musa ya umarta, Musa, Haruna
da Hur kuwa suka tafi bisa tudu. 11 Muddin hannun Musa yana a miƙe, sai Isra'ilawa
su yi ta cin nasara, amma da zarar hannunsa ya sauka, sai Amalekawa su yi ta cin
nasara. 12 Sa'ad da hannuwan Musa suka gaji, sai Haruna da Hur suka ɗauki dutse
suka sa ya zauna a kai. Sa'an nan su kuma suka tsaya gefe da gefe, suna riƙe da
hannuwansa har fāɗuwar rana. 13 Sai Yoshuwa kuwa ya ci nasara a kan Amalekawa
da takobi.
14 Sa'an nan UBANGIJI ya ce wa Musa, "Ka rubuta wannan a cikin littafi, yă zama
abin tuni, ka kuma faɗa wa Yoshuwa zan hallaka Amalekawa ƙaƙaf daga duniya."
15 Musa ya gina bagade, sai ya kira shi UBANGIJI shi ne Tutata. 16 Ya ce, "Gama
an ɗaga hannuwa sama zuwa kursiyin UBANGIJI, UBANGIJI zai yaƙi Amalekawa daga
tsara zuwa tsara."

# 18

*Yetro ya ziyarci Musa*

1 Ana nan sai Yetro firist na Midiyan, kuma surukin Musa, ya ji duk abin da Allah
ya yi wa Musa da mutanensa Isra'ila, da kuma yadda Ubangiji ya fitar da Isra'ila
daga Masar.
2 Bayan da Musa ya tura matarsa Ziffora gida, sai surukinsa Yetro ya karɓe ta 3 da
'ya'yanta biyu maza. Ana kira ɗaya Gershom, domin Musa ya ce, "Na zama baƙo a
baƙuwar ƙasa"; 4 ɗayan kuma Eliyezer, domin ya ce, "Allah mahaifina ya taimake ni
ya cece ni daga takobin Fir'auna."
5 Yetro surukin Musa tare da 'ya'yan Musa da matarsa suka zo wurin Musa a
hamada, inda suka kafa sansani kusa da dutsen Allah 6 Yetro ya riga ya aika wa
Musa cewa, "Ni surukinka Yetro, ina zuwa wurinka tare da matarka da 'ya'yanka
maza biyu."
7 Sai Musa ya tafi yă taryi surukinsa, ya sunkuya ya yi masa sumba. Suka gai da
juna, sa'an nan suka shiga tenti. 8 Musa kuwa ya faɗa wa surukinsa duk abubuwan
da Ubangiji ya yi wa Fir'auna da Masarawa domin Isra'ila, da batun wahalolin da
suka sha a hanya, da yadda Ubangiji ya cece su.
9 Yetro ya yi murna da jin duk abubuwa masu kyau da Ubangiji ya yi wa Isra'ila,
wajen cetonsu daga hannun Masarawa. 10 "Yabo ga Ubangiji wanda ya cece ku daga
hannun Masarawa da na Fir'auna, wanda kuma ya cece mutanensa daga hannun
Masarawa. 11 Yanzu na san cewa Ubangiji ya fi kowane allah, gama ya yi wannan
ga masu girman kai da kuma waɗanda suka wulaƙanta Isra'ila." 12 Sa'an nan Yetro
surukin Musa, ya kawo hadaya ta ƙonawa da waɗansu hadayu wa Allah, Haruna
ya zo tare da dukan dattawan Isra'ila, suka ci abinci tare da surukin Musa a gaban
Allah.

*(Maimaitawar Shari'a 1.9-18)*

13 Kashegari, Musa ya zauna domin yă yi wa mutane shari'a, sai suka tsaya kewaye
da shi daga safe har yamma. 14 Sa'ad da surukinsa ya lura da duk abin da Musa
yake yi saboda mutane, sai ya ce, "Mene ne wannan da kake yi wa mutane? Don me
kai kaɗai kake zama kana yin shari'a wa mutane, yayinda mutanen nan suke tsaya
kewaye da kai daga safe har yamma?"
15 Musa ya amsa ya ce, "Saboda mutanen suna zuwa wurina, don su nemi nufin
Allah. 16 Duk lokacin da suke da gardama, akan kawo su a wurina, ni kuma sai in
raba tsakaninsu, in kuma koya musu dokokin Allah da farillansa."
17 Surukin Musa ya amsa ya ce, "Abin da kake yi ba daidai ba ne. 18 Kai da dukan
mutanen da suke zuwa wurinka za ku gajiyar da kanku. Aikin ya fi ƙarfinka; ba za ka
iya yinsa kai kaɗai ba. 19 Ka kasa kunne gare ni yanzu, zan ba ka shawara, Allah kuma
yă kasance tare da kai. Kai za ka zama wakilin mutane a gaban Allah, ka kuma kawo
gardamansu gare shi. 20 Ka koya musu dokokinsa da farillarsa, ka kuma nuna musu
hanyar rayuwa da ayyukan da za su yi. 21 Amma ka zaɓi mutane masu iyawa daga
dukan mutane, maza masu tsoron Allah, amintattu, masu ƙin rashawa, ka sanya su
shugabanni na dubbai, ɗari-ɗari, hamsin-hamsin da goma-goma. 22 Bari waɗannan
mutane su sassanta mutane a kan ƙananan matsaloli, amma kowace babban matsala,
ko bukata ta musamman, sai su kawo wurinka, ƙananan matsaloli kuma sai su yanke
hukuncin da kansu. Ta haka ne za su taimaka wajen ɗaukan nauyin jama'a, don su
sa aikin yă zama maka da sauƙi. 23 In ka yi haka, Allah ya umarta za ka iya jimre
gajiyar, kuma dukan mutanen nan za su koma gida da murna."
24 Musa ya kasa kunne ga surukinsa, ya kuma aikata duk abin da ya faɗa. 25 Ya
zaɓi mutane masu iyawa daga cikin dukan Isra'ila, ya naɗa su shugabannin mutane,
shugabanni a kan dubbai, ɗari-ɗari, hamsin-hamsin da goma-goma. 26 Suka yi

hidimar alƙalanci na mutane a dukan lokaci. Gardandamin da suke da wuya, suka
kawo wurin Musa, amma ƙananan batuttuwa, suka shari'anta a tsakaninsu.
27 Sa'an nan Musa ya sallame surukinsa Yetro, ya kuwa koma ƙasarsa.

# 19

*A Dutsen Sinai*

1 A rana ta farko a cikin watan uku bayan da Isra'ilawa suka bar Masar, a wannan
rana, suka iso Hamadar Sinai. 2 Bayan da suka tashi daga Refidim, suka shiga
Hamadar Sinai, sai Isra'ilawa suka yi sansani a gaban dutsen.

3 Sai Musa ya hau kan dutsen don yă sadu da Allah, UBANGIJI kuwa ya kira shi daga
dutsen ya ce, "Wannan shi ne abin da za ka faɗa wa gidan Yaƙub, da kuma abin da
za ka faɗa wa mutanen Isra'ila. 4 'Ku da kanku kun ga abin da na yi wa Masar, da
yadda na ɗauko ku a kan fikafikan gaggafa na kawo ku wurina. 5 Yanzu, in kuka yi
mini cikakken biyayya, kuka kuma kiyaye yarjejjeniyata, to, za ku zama keɓeɓɓiyar
taska a gare ni a cikin dukan al'ummai. Ko da yake duk duniya tawa ce, 6 za ku
zama firistoci masu tsarki da kuma al'umma keɓaɓɓiya a gare ni.' Waɗannan su ne
kalmomin da za ka faɗa wa Isra'ilawa."
7 Sai Musa ya koma ya aika a kira dukan dattawan mutane, ya bayyana dukan
kalmomin da UBANGIJI ya umarta, ya faɗa. 8 Dukan mutane suka amsa gaba ɗaya
suka ce, "Za mu yi duk abin da UBANGIJI ya faɗa." Sai Musa ya mayar wa UBANGIJI
amsar da mutane suka bayar.

9 UBANGIJI kuwa ya ce wa Musa, "Ina zuwa wurinka a cikin baƙin hadari, domin
mutane su ji ni ina maganar da kai, domin su amince da kai koyaushe." Sa'an nan
Musa ya faɗa wa UBANGIJI abin da mutane suka ce.

10 Sai UBANGIJI ya ce wa Musa, "Tafi wurin mutanen, ka tsarkake su yau da gobe, ka
sa su wanke tufafinsu. 11 Su zama da shiri a rana ta uku, gama a ranar ce UBANGIJI zai
sauko a kan Dutsen Sinai a idon dukan mutane. 12 Sai ka yi wa jama'a iyaka kewaye
da dutsen, ka kuma faɗa musu cewa, 'Ku mai da hankali, kada ku hau dutsen ko ku
taɓa gefensa. Duk wanda ya taɓa dutsen, lalle za a kashe shi. 13 Za a jajjefe shi da
duwatsu, ko a harbe shi da kibiyoyi, ba hannun da zai taɓa shi. Mutum ko dabbar
da ya taɓa, ba za a bar shi da rai ba.' Lokacin da aka ji muryar ƙaho ne kawai za su
iya taru a gindin dutsen."

14 Bayan da Musa ya gangara wurin mutane, ya tsarkake su, sai suka wanke
tufafinsu. 15 Sa'an nan ya ce wa mutane, "Ku shirya kanku domin rana ta uku. Ku
ƙame kanku daga yin jima'i."

16 A safiyar rana ta uku, aka yi tsawa, da walƙiyoyi, sai ga girgije mai duhu a bisa
dutsen, aka tsananta busar ƙaho, sai dukan jama'ar da suke cikin sansani suka yi
rawar jiki. 17 Sa'an nan Musa ya jagoranci mutane daga sansani domin su sadu da
Allah, sai suka tsaya a gefen dutsen. 18 Dutsen Sinai kuwa ya tunnuƙe duka da hayaƙi,
gama UBANGIJI ya sauko a bisan dutsen cikin wuta. Hayaƙin ya hau kamar hayaƙin
da yake fitowa daga matoya, duk dutsen ya yi rawa da ƙarfi, 19 sai karar ƙaho ya yi
ta ƙaruwa. Sa'an nan Musa ya yi magana, murya Allah kuwa ta amsa masa.

20 UBANGIJI ya sauko a kan ƙwanƙolin Dutsen Sinai, ya kira Musa zuwa ƙwanƙolin
dutsen. Musa kuwa ya haura 21 sai UBANGIJI ya ce masa, "Ka sauka ka faɗa wa jama'a,
kada su kuskura su ƙetare layin iyakan nan, garin son zuwa don ganin UBANGIJI,
gama duk waɗanda suka yi haka za su mutu. 22 Ko firistocin da za su kusato UBANGIJI
sai su tsarkake kansu, don kada in hallaka su."

23 Musa ya ce wa UBANGIJI, "Mutanen ba za su hau Dutsen Sinai ba, gama kai da
kanka ka gargaɗe mu, 'Ku sa iyaka kewaye da dutsen ku kuma tsarkake shi.' "

24 UBANGIJI ya amsa, "Sauka ka kawo Haruna tare da kai. Amma kada firistoci da mutane su zarce iyakan nan, a kan za su zo wurin UBANGIJI, don kada in hallaka su."
25 Saboda haka Musa ya sauka wurin mutane ya kuma faɗa musu.

# 20

*Dokoki goma*
*(Maimaitawar Shari'a 5.1-21)*

1 Sai Allah ya faɗi waɗannan kalmomi ya ce,

2 "Ni ne UBANGIJI Allahnka, wanda ya fitar da ku daga Masar, daga ƙasar bauta.

3 "Ba za ka yi wa kanka waɗansu alloli ba sai ni.
4 Ba za ka yi wa kanka waɗansu alloli a siffar wani abu a sama a bisa, ko a
ƙarƙashin ƙasa, ko a ƙarƙashin ruwa ba. 5 Ba za ka durƙusa gare su, ko ka yi
musu sujada ba. Gama ni, UBANGIJI Allahnka mai kishi ne, nakan hukunta 'ya'ya
har tsara ta uku da ta huɗu na waɗanda suke ƙina, 6 amma ina nuna ƙauna ga
tsara dubbai na waɗanda suke ƙaunata, suke kuma kiyaye umarnaina.
7 Ba za ka yi amfani da sunan UBANGIJI Allahnka a banza ba, gama UBANGIJI zai hukunta duk wanda ya mai da sunansa banza.
8 Ka tuna da ranar Asabbaci domin ka kiyaye ta da tsarki. 9 Kwana shida za ka yi
dukan aikinka, 10 amma rana ta bakwai Asabbaci ne ga UBANGIJI, Allahnka. A
ranar ba za ka yi wani aiki ba, ko kai, ko ɗanka, ko 'yarka, ko bawa, ko baiwa,
ko dabbarka, ko baƙon da yake zama tare da kai. 11 Gama kwana shida UBANGIJI
ya halicci sama da ƙasa, da teku, da duk abin da yake cikinsu, amma ya huta a rana ta bakwai. Saboda haka UBANGIJI ya albarkaci ranar Asabbaci, ya kuma mai da ita mai tsarki.
12 Ka girmama mahaifinka da mahaifiyarka, domin ka yi tsawon rai a ƙasar da UBANGIJI Allahnka yake ba ka.
13 Ba za ka yi kisankai ba.
14 Ba za ka yi zina ba.
15 Ba za ka yi sata ba.
16 Ba za ka ba da shaidar ƙarya a kan maƙwabcinka ba.
17 Ba za ka yi ƙyashin gidan maƙwabcinka ba. Ba za ka yi ƙyashin matar maƙwabcinka ba, ko bawansa, ko baiwarsa, ko sansa, ko jakinsa, ko duk abin da yake na maƙwabcinka ba."

*(Maimaitawar Shari'a 5.23-33)*

18 Da mutane suka ga tsawa da walƙiya, suka ji karar ƙaho, suka kuma ga dutsen
yana hayaƙi, sai suka yi rawar jiki don tsoro. Suka tsaya da nisa 19 suka ce wa Musa,
"Ka yi magana da mu da kanka, za mu kasa kunne. Amma kada Allah ya yi mana magana, don kada mu mutu."
20 Musa ya ce wa mutane, "Kada ku ji tsoro, gama Allah ya zo don yǎ gwada ku, don ku riƙa girmama shi, don kuma kada ku yi zunubi."
21 Sa'ad da mutane suka tsattsaya da nesa, sai Musa ya matsa kusa da girgije mai duhu, inda Allah yake.

*Gumaka da bagadai*

22 Sa'an nan UBANGIJI ya ce wa Musa, "Ka faɗa wa Isra'ilawa wannan. 'Kun gani
da kanku cewa na yi magana da ku daga sama. 23 Kada ku yi waɗansu alloli in ban
da ni, kada ku yi wa kanku allolin azurfa ko na zinariya.

[24] “ ‘Ku yi mini bagaden ƙasa, ku kuma miƙa mini hadaya ta ƙonawa da hadaya
ta salama, za ku hadayar da tumakinku da awakinku da shanu. Duk inda na
sa a girmama sunana, zan zo wurinku, in sa muku albarka. [25] In kuka yi mini
bagade dutse, kada ku gina shi da sassaƙaƙƙun duwatsu, gama inda guduma ta taɓa
duwatsun, sun haramtu ke nan. [26] Kada ku gina wa bagadena matakala, domin kada
yayinda wani yana hawa, mutane su ga tsiraicinsa.’

# 21

*(Maimaitawar Shari’a 15.12-18)*
[1] “Waɗannan su ne dokokin da za ka sa a gabansu.

*Bayin Ibraniyawa*
[2] “In ka sayi mutumin Ibraniyawa a matsayin bawa, zai bauta maka shekara shida.
Amma a shekara ta bakwai, za ka ’yantar da shi, yă tafi ’yantacce, ba tare da ya biya
kome ba. [3] In ya zo shi kaɗai, zai tafi ’yantacce shi kaɗai; amma in yana da mata a
lokacin da ya zo, za tă tafi tare da shi. [4] In maigidansa ya yi masa aure, ta kuwa haifa
masa ’ya’ya maza ko mata, matan da ’ya’yan, za su zama na maigidan, sai mutumin
kaɗai zai tafi ’yantacce.
[5] “Amma in bawan ya furta ya ce, ‘Ina ƙaunar maigidana, da matata, da ’ya’yana,
ba na so kuma in ’yantu,’ [6] dole maigidansa yă kai shi gaban alƙalai. Zai kai shi ƙofa
ko madogarar ƙofa, yă huda kunnensa da basilla, sa’an nan zai zama bawansa duk
tsawon kwanakinsa a duniya.
[7] “In mutum ya sayar da ’yarsa a matsayin baiwa, ba za a ’yantar da ita kamar
bawa ba. [8] In ba tă gamshi maigida wanda ya zaɓe ta domin kansa ba, dole yă bari
a fanshe ta. Ba shi da dama yă sayar da ita ga baƙi, tun da yake bai kyauta mata ba.
[9] In ya zaɓe ta domin ɗansa, dole yă ba ta duk damar da ’ya ta mace take da shi. [10] In
ya auri wata mace, ba zai hana wa baiwar abinci da sutura ba, ba kuma zai ƙi kwana
da ita ba. [11] In bai tanada mata waɗannan abubuwa uku ba, sai tă tafi ’yantacciya,
babu biyan kome.

*Jin rauni*
[12] “Duk wanda ya bugi mutum har ya kashe shi, lalle a kashe shi. [13] Amma in ba
da nufin yă kashe shi ba, sai dai in Allah ne ya nufa haka, to, sai mutumin yă tsere
zuwa inda zan nuna muku. [14] Amma in mutumin ya yi dabara har ya kashe wani
mutum da gangan, sai a ɗauke shi daga bagadena a kashe shi.
[15] “Duk wanda ya bugi mahaifinsa ko mahaifiyarsa, dole a kashe shi.
[16] “Duk wanda ya saci mutum ya sayar da shi, ko kuwa aka iske shi a hannunsa,
lalle kashe shi za a yi.
[17] “Duk wanda ya la’anta mahaifinsa ko mahaifiyarsa, dole a kashe shi.
[18] “Idan mutane suka yi faɗa, ɗayan ya jefa ɗayan da dutse, ko ya naushe shi amma
bai mutu ba, sai dai ya yi ta jiyya, [19] idan mutumin ya sāke tashi ya yi tafiya ko da
yana dogarawa da sanda ne, wanda ya buge shi zai kuɓuta, sai dai zai biya diyyar
lokacin da ya ɓata masa, yă kuma lura da shi, har yă warke sarai.
[20] “In mutum ya dūke bawansa ko baiwarsa da sanda, sai bawan ko baiwar ta
mutu saboda dūkan, dole a hukunta shi, [21] amma ba za a hukunta shi ba, in bawan
ko baiwar ta tashi, bayan kwana ɗaya ko biyu, tun da bawan ko baiwar mallakarsa
ne.
[22] “Idan mutum biyu suna faɗa, har suka yi wa mace mai ciki rauni, har ya sa ta yi
ɓari, amma wani lahani bai same ta ba, za a ci wa wanda ya yi mata raunin tara bisa
ga yadda mijinta ya yanka za a biya, in dai abin da ya yanka ya yi daidai da abin da
alƙalai suka tsara. [23] Amma in akwai rauni mai tsanani, sai a ɗauki rai a maimakon

rai, 24 ido don ido, haƙori don haƙori, hannu don hannu, ƙafa don ƙafa, 25 ƙuna don
ƙuna, rauni don rauni, ƙujewa don ƙujewa.
26 “In mutum ya bugi bawa ko baiwa a ido, har idon ya lalace, dole yă ʼyantar da
shi ko ita, maimakon ido. 27 In kuma ya fangare haƙorin bawa ko baiwa, dole yă
ʼyantar da bawan ko baiwar, a maimakon haƙorin.
28 “In bijimi ya kashe namiji ko ta mace, dole a jajjefe bijimin har yă mutu, ba za a
kuma ci namansa ba. Amma mai bijimin ba shi da laifi. 29 In, har an san bijimin da
wannan hali, an kuma yi wa mai shi gargaɗi, amma bai ɗaura shi ba, har ya kashe
namiji ko ta mace, za a jajjefe bijimin tare da mai shi, har su mutu. 30 Amma fa, in
an bukace shi yă biya, zai biya don yă fanshi ransa ta wurin biyan abin da aka aza
masa. 31 Wannan doka ta shafi batun bijimin da ya kashe ɗa ko ʼya. 32 In bijimin ya
kashe bawa ko baiwa, mai shi zai biya shekel talatin na azurfa wa maigidan bawan,
a kuma a jajjefe bijimin.
33 “In mutum ya bar rami a buɗe, ko ya haƙa rami bai kuma rufe ba, sai saniya
ko jaki ya fāɗi a ciki, 34 Mai ramin zai biya rashin da aka yi wa mai shi, matacciyar
saniyan ko jakin, zai zama na mai ramin.
35 “In bijimin mutum ya raunana bijimin wani, har ya mutu, sai mutanen biyu su
sayar da mai ran, su raba kuɗin daidai, haka ma su yi da mai ran. 36 Amma fa, in
tun can, an san bijimin yana da wannan halin faɗa, duk da haka mai shi bai ɗaura
shi ba, dole mai shi yă biya, dabba domin dabba, matacciyar dabbar kuwa tă zama
nasa.

# 22

*Tsarewar mallaka*
1 “In mutum ya saci saniya ko tunkiya ya yanka, ko ya sayar, zai biya shanu biyar,
a maimakon saniyar da ya sata, ko kuma tumaki huɗu, maimakon tunkiyar da ya
sata.
2 “In aka iske ɓarawo yana cikin ƙoƙarin shiga yă yi sata, aka buge shi har ya
mutu, to, ba za a nemi alhakin jininsa daga wurin kowa ba; 3 amma in ya faru bayan
wayewar gari, to, za a nemi alhakin jinin ɓarawon a hannun wanda ya bugi ɓarawon.
“Ɓarawon da aka kama da abin da ya sata, dole yă yi cikakkiyar ramuwa, amma
in ba shi da kome, dole a sayar da shi a biya abin da ya sata. 4 In an sami dabbar, ko
saniya, ko jaki, ko tunkiya da ya sata da rai a hannunsa, dole ɓarawon yă biya taran
da za a ci shi, sau biyu na kowane ɗaya.
5 “In mutum ya sa dabbobinsa su yi kiwo a fili ko a gonar inabi, ya kuma bar
dabbobinsa suka yi ɓarna a cikin gonar wani, sai a sa mai dabbar yă biya tara daga
amfanin gonarsa mafi kyau duka.
6 “In gobara ta tashi, ta kuma bazu cikin ƙayayyuwa, har ta cinye tarin hatsi, ko
hatsin da ke tsaye, ko dukan gonar, dole wanda ya sa wutar, yă biya taran da aka
yanka masa saboda ɓarnan da wutar ta yi.
7 “In mutum ya ba maƙwabcinsa azurfa, ko kaya ajiya, aka kuma sace su daga
gidan maƙwabcin, in an kama ɓarawon, sai ɓarawon yă biya abin da ya sata har
sau biyu. 8 Amma in ba a sami ɓarawon ba, sai wanda aka yi ajiyar a gidansa, yă
bayyana a gaban alƙalai a bincika ko yana da hannu a kan kayan maƙwabcinsa. 9 A
kowane rikicin cin amana da zai shiga tsakanin mutum biyu, ko a kan bijimi, ko jaki,
ko tunkiya, ko riga, kai, ko a kan kowane irin abin da ya ɓata, da ma abin da aka
samu a hannun wani, in akwai jayayya, za a kawo mutumin a gaban alƙalai. Wanda
alƙali ya ce shi ne mai laifi, sai yă biya ɗayan taran da za a yanka, har sau biyu.
10 “In mutum ya ba da jaki, ko saniya, ko tunkiya, ko kowace dabba wa
maƙwabcinsa ajiya, sai abin ya mutu, ko ya ji rauni, ko an ɗauke shi, in ba shaida,
11 rantsuwa ce za tă raba tsakaninsu a gaban Ubangiji cewa babu hannunsa a dukiyar

maƙwabcinsa. Mai dukiyar kuwa zai yarda da rantsuwar, ba za a bukaci wanda aka
bai wa amanar yă biya ba. 12 Amma idan satan dabbar ce aka yi, dole wanda aka bai
wa ajiyar yă biya mai dabbar taran da aka ci masa. 13 In naman jeji ne ya kashe ta,
zai nuna gawar don shaida, ba za a kuwa sa maƙwabcin yă biya abin da naman jeji
ya kashe ba.
14 "In mutum ya yi aron dabba daga wurin maƙwabcinsa, sai dabbar ta ji rauni ko
ta mutu, yayinda mai shi ba ya nan, dole wanda ya yi aron dabbar yă biya. 15 Amma
idan mai dabbar yana a wurin, wanda ya karɓa aron, ba zai biya kome ba. In an yi
hayar dabbar ce, to, kuɗin da aka biya na hayar zai zama a madadin rashin.

*Hakkin zamantakewa*

16 "Idan mutum ya ruɗe budurwa, wadda ba wanda yake nemanta, ya kuma
kwanta da ita, dole yă biya kuɗin aurenta, za tă kuma zama matarsa. 17 In mahaifinta
ya ƙi yă ba da ita ga mutumin, dole mutumin yă biya dukiya daidai da abin da akan
biya domin budurwai.
18 "Kada ku bar maiya da rai.
19 "Duk mutumin da ya yi jima'i da dabba dole a kashe shi.
20 "Duk wanda ya yi hadaya ga wani allah ban da UBANGIJI, dole a hallaka shi.
21 "Kada a wulaƙanta, ko a zalunci baƙo, domin dā ku baƙi ne a ƙasar Masar.
22 "Kada ku ci zalin gwauruwa, ko maraya. 23 In kuka yi haka, idan kuma suka yi
kuka gare ni, zan ji kukansu. 24 Zan husata, in kuma kashe ku da takobi; matanku
kuma, su ma su zama gwauraye, 'ya'yanku kuwa su zama marayu.
25 "In kun ba wa jama'ata matalauta da suke tsakaninku bashin kuɗi, kada ku
zama kamar masu ba da rance; kada ku sa yă biya da ruwa. 26 In kun ɗauki mayafi
maƙwabcinku a matsayin jingina, ku mayar masa kafin fāɗuwar rana, 27 domin
mayafin ne abin da yake da shi na rufe jikinsa. To, da me zai rufu yă yi barci?
Sa'ad da ya yi mini kuka, zan ji, gama ni mai tausayi ne.
28 "Kada ku yi maganar saɓo ga Allah, ko ku la'anta mai mulkin mutanenku.
29 "Kada ku jinkirta fitar da zakarku daga rumbunanku, ko harajin kayan da kuka
saya.
"Dole ku ba ni 'ya'yan farinku maza. 30 Ku yi haka da shanunku da tumakinku.
Bari su kasance da iyayensu mata, har kwana bakwai, amma ku ba ni su a rana ta
takwas.
31 "Za ku kasance mutanena masu tsarki. Saboda kada ku ci naman da namun jeji
suka kashe; ku jefa wa karnuka.

# 23

*Dokokin adalci da jinƙai*

1 "Kada ku baza rahoton ƙarya. Kada kuma ku haɗa baki da mugayen mutane har
da ku zama munafukai ta wurin ba da shaidar ƙarya.
2 "Kada ku yi abin da ba daidai ba, don galibin mutane suna yin haka. Sa'ad da
kuke ba da shaida a gaban shari'a, kada ku ba da shaidar ƙarya a kauce wa gaskiya
don ku faranta wa taron jama'a rai. 3 Kada ku yi wa matalauci sonkai a gaban shari'a.
4 "In ka ga saniyar abokin gābanka, ko jakinsa ya ɓace, ka yi ƙoƙari ka mai da shi
wurinsa. 5 In ka ga jakin wani maƙiyinka ya fāɗi a ƙarƙashin kayan da ya ɗauka,
kada ka bar shi can, ka yi ƙoƙari ka taimake shi.
6 "Kada ku kāsa yin adalci ga matalauci a wurin shari'a. 7 Ku yi nesa da ƙage.
Kada ku kashe marar laifi tare da mai adalci, gama ba zan bar mugun yă tafi haka
kawai ba.
8 "Kada ka karɓi cin hanci, gama cin hanci yakan makanta waɗanda suke gani,
yakan kuma karkatar da maganar masu adalci.

9 “Kada ka zalunci baƙo, ku kanku kun san halin baƙunci, gama dā ku baƙi ne a Masar.

*Dokokin Asabbaci*

10 “Shekara shida za ku nome gonakinku ku girbe amfanin gonar, 11 amma a shekara
ta bakwai za ku bar ƙasa tă huta. Sa'an nan matalautan da suke cikinku za su sami abinci daga cikinta, namun jeji kuma za su ci abin da aka bari. Ku yi haka da gonakinku na inabi, da na itatuwan zaitun.

12 “Kwana shida za ku yi aikinku, amma a rana ta bakwai, kada ku yi aiki, saboda saniyarku da jakinku su huta, haka kuma bawan da aka haifa a gidanku, da kuma baƙon da yake a cikinku yă wartsake.

13 “Ku mai da hankali, ku yi biyayya da duk abin da na faɗa muku. Kada ku kira sunaye waɗansu alloli; kada a ji su a bakinku.

*Bukukkuwa uku na shekara*
*(Fitowa 34.18-26; Maimaitawar Shari'a 16.1-17)*

14 “Sau uku a shekara za ku yi mini biki.

15 “Ku yi Bikin Burodi Marar Yisti, kwana bakwai za ku ci burodi marar yisti, kamar yadda na umarce ku. Ku yi wannan a lokacin da aka ayana a watan Abib, gama a watan ne kuka fito daga Masar.

“Kada wani yă zo a gabana hannu wofi.

16 “Ku yi Bikin Girbi da nunan fari na amfanin shuke-shuken gonarku.

“Ku yi Bikin Tattarawa a ƙarshen shekara, sa'ad da kuka tattara amfani daga gonarku.

17 “Sau uku a shekara, maza duka za su bayyana a gaban Ubangiji Mai Iko Duka.

18 “Kada ku miƙa mini hadayar jini tare da wani abu mai yisti.

“Ba za a bar kitsen bikin hadayata yă kwana ba.

19 “Dole ne ku kawo mafi kyau daga nunan fari na gonakinku a gidan Ubangiji Allahnku.

“Kada ku dafa ɗan akuya a cikin madarar mahaifiyarsa.

*Mala'ikan Allah zai shirya hanya*

20 “Ga shi, zan aika mala'ika a gabanku, yă tsare ku a tafiyarku, yă kuma kawo ku
wurin da na shirya. 21 Ku saurare shi, ku kuma kasa kunne ga abin da yake faɗa. Kada
ku yi masa tawaye; ba zai gafarta tawayenku ba, gama shi wakilina ne. 22 In kun kasa
kunne sosai ga abin da yake faɗi, kuka kuma yi abin da na faɗa, zan zama magabci ga
abokan gābanku, zan kuma yi hamayya da abokan hamayyanku. 23 Mala'ikana zai
sha gabanku, yă kawo ku cikin ƙasar Amoriyawa, da Hittiyawa, da Ferizziyawa, da
Kan'aniyawa, da Hiwiyawa, da kuma Yebusiyawa, zan kuma kawar da su. 24 Kada ku
durƙusa wa allolinsu, ko ku yi musu sujada, ko kuma ku bi al'adunsu. Za ku hallaka
dukan allolinsu, ku kuma farfasa keɓaɓɓun duwatsunsu. 25 Ku bauta wa Ubangiji
Allahnku, albarkansa kuwa za tă kasance a kan abincinku da ruwan shanku. Zan
ɗauke cuta daga cikinku. 26 A ƙasarku, mace ba za tă yi ɓari ba, ba kuma za a sami
marar haihuwa ba. Zan ba ku tsawon rai.

27 “Zan aiki razanata a gabanku, in kuma sa ruɗami a cikin kowace al'ummar da
za ku sadu da ita. Zan sa duk abokan gābanku su juye da baya, su gudu. 28 Zan aiki
rina a gabanku, su kori Hiwiyawa, Kan'aniyawa da kuma Hittiyawa. 29 Amma ba a
shekara guda zan kore muku su ba, don kada ƙasar tă zama kufai har namun jeji su
fi ƙarfinku. 30 Da kaɗan da kaɗan zan kore muku su, har yawanku yă kai yadda za
ku mallaki ƙasar.

31 “Zan kafa iyakokinku daga Jan Teku* zuwa Bahar Rum,† daga hamada kuma
zuwa Kogi.‡ Zan ba da mazaunan ƙasar a hannunku, za ku kuwa kore su daga
gabanku. 32 Kada ku ƙulla yarjejjeniya da su, ko da allolinsu. 33 Kada ku bari su
zauna a cikin ƙasarku, in har kuka bar su, za su ɓata ku da zunubinsu na bautar
allolinsu, har zai yă zama muku tarko.”

# 24

*An Tabbatar da alkawari*
1 Ana nan sai UBANGIJI ya ce wa Musa, “Ku hauro zuwa wurina, kai da Haruna,
Nadab da Abihu, da kuma dattawa saba’in a cikin Isra’ila. Za ku yi sujada da ɗan
nisa, 2 sai Musa kaɗai zai kusaci UBANGIJI. Amma sauran kada su zo kusa, kada kuma
jama’a su hau tare da shi.”
3 Sa’ad da Musa ya tafi ya faɗa wa mutanen duk kalmomin UBANGIJI da dokokinsa,
sai suka amsa da murya ɗaya suna cewa, “Duk abin da UBANGIJI ya faɗa, za mu yi.”
4 Sai Musa ya rubuta duk abin da UBANGIJI ya faɗa.
Ya tashi kashegari da sassafe ya gina bagade kusa da dutsen, ya aza al’amudai goma
sha biyu bisa ga kabilu goma sha biyu na Isra’ila. 5 Sai ya aiki samarin Isra’ilawa, suka
miƙa hadaya ta ƙonawa, suka kuma miƙa ƙananan bijimai don hadaya ta salama ga
UBANGIJI. 6 Musa ya ɗauki rabin jinin ya zuba a cikin kwanoni, rabin kuma ya yayyafa
a kan bagaden. 7 Sa’an nan ya ɗauki Littafin Alkawari ya karanta wa mutane. Suka
amsa suka ce, “Za mu yi duk abin da UBANGIJI ya faɗa; za mu yi biyayya.”
8 Musa ya kuma ɗauki jinin, ya yayyafa a kan mutanen ya ce, “Wannan shi ne jinin
alkawarin da UBANGIJI ya yi da ku, bisa ga dukan waɗannan kalmomi.”
9 Musa da Haruna, Nadab da Abihu, da dattawa saba’in, Allah na Isra’ila suka haura
10 suka kuma ga Allah na Isra’ila. A ƙarƙashin ƙafafunsa akwai wani abu wanda aka
yi da saffaya, mai haske kuma kamar sararin sama kansa. 11 Amma Allah bai yi wa
shugabannin Isra’ila wani abu ba; suka ga Allah, suka ci suka kuma sha.
12 UBANGIJI ya ce wa Musa, “Hauro wurina a kan dutse, ka tsaya a nan, zan ba ka
allunan dutsen, da doka da umarnan da na rubuta don koyonsu.”
13 Sa’an nan Musa ya fita tare da Yoshuwa mataimakinsa, ya kuwa hau kan dutsen
Allah. 14 Ya ce wa dattawan, “Ku jira mu a nan, sai mun dawo wurinku. Haruna da
Hur suna tare da ku, in wani yana da wata damuwa, sai yă je wurinsu.”
15 Da Musa ya hau dutsen, sai girgije ya rufe dutsen, 16 sai ɗaukakar UBANGIJI ta
sauka a kan Dutsen Sinai, kwana shida girgije ya rufe dutsen, a rana ta bakwai, sai
UBANGIJI ya kira Musa daga cikin girgijen. 17 Ga Isra’ilawa dai, ɗaukakar UBANGIJI ta
yi kamar wuta mai ci a kan dutse. 18 Sa’an nan Musa ya shiga girgijen ya hau kan
dutsen. Ya zauna a kan dutsen yini arba’in da dare arba’in.

# 25

*Hadayu don tabanakul*
*(Fitowa 35.4-9)*
1 UBANGIJI ya ce wa Musa, 2 “Ka faɗa wa Isra’ilawa su kawo mini hadaya. Za ka
karɓi hadaya daga hannun kowane mutum wanda zuciyarsa ta yarda yă bayar.

3 “Ga iri jerin kayan da za ka karɓo daga hannunsu,

“zinariya, da azurfa, tagulla,
4 shuɗi, shunayya da jan zare, lallausan lilin,

* 23:31 Da Ibraniyanci Yam Suf; wato, Tekun Iwa. † 23:31 Wato, Mediterraniyan ‡ 23:31 Wato, Yuferites

da gashin akuya,
5 fatun ragunan da aka wanke, fatun awaki masu kyau,
itacen akashiya,
6 mai domin fitila,
kayan yaji domin man keɓewa da kuma turare mai ƙanshi,
7 da duwatsun Onis, da duwatsun da za a mammanne a efod da ƙyallen maƙalawa a ƙirji.

8 “Sa’an nan ka sa su yi mini wuri mai tsarki, domin in zauna a cikinsu. 9 Ka ƙera
wannan tabanakul da duk kayan da suke ciki da waje, daidai yadda zan nuna maka.

*Akwatin alkawari*
*(Fitowa 37.1-9)*

10 “Ka sa a yi akwatin alkawarin da itacen ƙirya, tsawonsa kamu biyu da rabi,
fāɗinsa kamu ɗaya da rabi, tsayinsa kuma kamu ɗaya da rabi. 11 Ka dalaye shi da
zinariya zalla ciki da waje, za ka yi wa gefe-gefensa ado da gurun zinariya. 12 Ka
kewaye akwatin da zoban zinariya huɗu ka kuma haɗa su da ƙafafunsa huɗu,
zobai biyu a kowane gefe. 13 Sa’an nan ka yi sanduna da itacen ƙirya, ka dalaye
su da zinariya. 14 Ka sa sandunan a cikin zoban, a gefen akwatin domin ɗaukansa.
15 Sanduna za su kasance a cikin waɗannan zoban akwatin alkawarin; ba za a cire
su ba. 16 Sa’an nan ka sa Shaidar da zan ba ka, a cikin akwatin.
17 “Ka yi murfin kafara da zinariya zalla, tsawonsa kamu biyu da rabi, fāɗinsa
kuma kamu ɗaya da rabi. 18 Ka kuma yi kerubobi biyu da zinariyar da aka ƙera, ka
sa a gefen nan biyu na murfin. 19 Ka yi kerubobi biyu, ɗaya a wannan gefe, ɗaya
kuma a ɗayan gefen; za ka manne su a kan murfin, su zama abu ɗaya. 20 Kerubobin
su kasance da fikafikansu a buɗe, domin su inuwantar da murfin, za su fuskanci
juna, suna duba murfin. 21 Ka sa murfin a bisa akwatin ka kuma sa allunan dokokin
alkawarin da zan ba ka a ciki. 22 Can, a bisa murfin da yake tsakanin kerubobi biyu
da suke bisa akwatin alkawari na Shaida, zan sadu da kai, in kuma ba ka dukan
umarnai domin Isra’ilawa.

*Tebur*
*(Fitowa 37.10-16)*

23 “Ka yi tebur da itacen ƙirya, tsawonsa kamu biyu, fāɗinsa kamu ɗaya, tsayinsa
kuma kamu ɗaya da rabi. 24 Ka dalaye shi da zinariya zalla ka kuma yi masa ado
kewaye da gurun zinariya. 25 Ka yi dajiya mai fāɗin tafin hannu, ka kuma yi wa
dajiyar ado da gurun zinariya. 26 Ka yi zoban zinariya huɗu domin teburin, ka daure
su a kusurwoyi huɗu, inda ƙafafu huɗun suke. 27 Zoban za su kasance kusa da dajiyar
don riƙe sandunan da za a yi amfani don ɗaukar teburin. 28 Ka yi sandunan da itacen
ƙirya, ka dalaye su da zinariya, da sandunan ne za ku riƙa ɗaukan teburin. 29 Da
zinariya zalla kuma za ka yi farantansa, da kwanoninsa na tuya, da butocinsa, da
kwanoninsa domin zuban hadayu. 30 Ka sa burodin Kasancewa a kan wannan tebur,
yă kasance a gabana kullum.

*Wurin ajiye fitila*
*(Fitowa 37.17-24)*

31 “Ka yi wurin ajiye fitilar da zinariya zalla, ka kuma yi gindinsa tare da gorar
jikinsa da ƙerarriyar zinariya; kwafunansa da suka yi kamar furanni, tohonsa da
furanninsa su yi yadda za su zama ɗaya da shi. 32 Wurin ajiye fitilar yă kasance da
rassa shida, rassan nan za su miƙe daga kowane gefe na wurin ajiye fitilan, uku a
gefe guda, uku kuma a ɗaya gefen. 33 Kwafuna uku masu siffar furanni almon, da
toho, da kuma furannin za su kasance a rashe guda, uku a kan rashe na biye, haka

kuma a kan saura rassan shida da suka miƙe daga wurin ajiye fitilan. 34 A bisa wurin
ajiye fitilan kuwa za a kasance da kwafuna huɗu masu siffar furannin almon, da
toho, da furanni. 35 Toho ɗaya zai kasance a ƙarƙashin rassa biyu na farkon da suka
miƙe daga wurin ajiye fitilan, toho na biyu a ƙarƙashin rassa biyu na biye, toho na
uku a ƙarƙashin rassa na uku, rassa shida ke nan duka. 36 Tohon da kuma rassan za
su kasance ɗaya da wurin ajiye fitilan da aka yi da ƙerarriyar zinariya.

37 "Sa'an nan ka yi fitilu bakwai, ka sa su a bisa wurin ajiye fitilan ta yadda za
su haskaka wajen da suka fuskanta. 38 Za a yi lagwaninsa da manyan farantansa da
ƙerarriyar zinariya. 39 Da zinariya zalla na talenti ɗaya za ka yi wurin ajiye fitilan
da waɗannan abubuwa duka. 40 Sai ka lura ka yi su daidai bisa ga fasalin da aka
nuna maka a kan dutse.

# 26

*Tabanakul*
*(Fitowa 36.8-19)*

1 "Ka yi tabanakul da labule goma na lilin mai laushi a naɗe shi biyu, a saƙa labulen
da ulu mai ruwan shuɗi, da ulu mai ruwan shunayya, da kuma ulu mai ruwan ja.
Waɗannan labule za a yi musu zānen siffofin kerubobi, aikin gwani. 2 Dukan labulen,
girmansu zai zama kamu ashirin da takwas, fāɗinsu kuwa kamu huɗu. Labulen su
zama daidai wa daida. 3 Ka haɗa labule biyar tare, ka yi haka kuma da suran biyar
ɗin. 4 Ka sa wa labulen rammuka da ulu mai ruwan shuɗin a gefen ƙarshe na labule
ɗaya, a kuma yi haka a ƙarshen gefe na ɗaya kuma. 5 Ka yi wa labulen rammuka
hamsin a ɗayan labule, ka kuma yi haka a ƙarshe ɗayan labulen, rammukan su
fuskanci juna. 6 Sa'an nan ka yi maɗauri hamsin na zinariya don amfanin ɗaura
labulen a haɗe, domin tabanakul yă zama ɗaya.

7 "Ka yi labule goma sha ɗaya na gashin akuya da za ka rufe tabanakul. 8 Tsawon
kowanne yă zama kamu talatin, fāɗinsa kuma yă zama kamu huɗu. Labulen za su
zama daidai wa daida. 9 Ka haɗa labule biyar ka ɗinka. Haka kuma za ka yi da sauran
shidan. Ka naɗe shida ɗin biyu, ka yi labulen ƙofar tentin da shi. 10 Ka yi rammuka
hamsin a ƙarshen gefen kashi ɗaya na labulen, haka kuma a ƙarshen kashi ɗayan.
11 Sai ka kuma yi maɗauri hamsin da tagulla, ka ɗaura su a haɗe da tentin su zama
ɗaya. 12 Ragowar rabin labulen da yake a bisa tenti kuma sai a bar shi yana lilo a
bayan tabanakul. 13 Tsawon labulen tenti zai zama kamu ɗaya a kowane gefe, abin
da ya rage kuma sai a bar shi ya yi ta lilo a kowane gefe don yă rufe tabanakul. 14 Ka
yi abin rufe tentin da fatun raguna da aka rina ja, a kansa kuma ka rufe shi da fatun
shanun teku.

*(Fitowa 36.20-34)*

15 "Ka yi tabanakul da katakon itacen ƙiryar da aka kakkafa a tsaye. 16 Tsawon
kowane katako zai zama kamu goma, fāɗinsa kuma kamu ɗaya da rabi, 17 ka kafa
katakan suna duban juna. Ka yi da dukan katakan tabanakul haka. 18 Ka shirya
katakai ashirin a gefen kudu na tabanakul, 19 ka kuma yi rammuka arba'in da azurfar
da za a sa wa katakan nan ashirin. Za a sa kawunan katakan da aka fiƙe a cikin
rammukan. 20 Game da ɗayan gefen, gefen arewa na tabanakul, za ka kafa katakai
ashirin, 21 da rammukan azurfa arba'in, biyu a ƙarƙashin kowane katako. 22 Ka kafa
katakai shida don can ƙarshen katakan, wato, a wajen yamma na ƙarshen tabanakul,
23 ka kuma kafa katakai biyu a kusurwoyi can ƙarshe. 24 Za a haɗa katakan nan a
kusurwa daga ƙasa zuwa sama a daure su. Haka za a yi da katakan kusurwa na biyu.
25 Ta haka za a sami katakai takwas da rammukansu na azurfa guda goma sha shida,
kowane katako yana da rammuka biyu.

26 “Ka kuma yi sanduna da itacen ƙirya. Sanduna biyar domin katakai na gefe ɗaya
na tabanakul, 27 biyar domin katakai wancan gefe, biyar kuma domin na gefe wajen
yamma, can ƙarshen tabanakul. 28 Sandan da yake tsakiyar katakan, zai bi daga
wannan gefe zuwa ƙarshen wancan gefe. 29 Ka dalaye dukan katakan da zinariya,
ka kuma yi zoban zinariya don su riƙe sandunan. Ka kuma dalaye sandunan da
zinariya.
30 “Ka yi tabanakul bisa ga fasalin da aka nuna maka a bisa dutsen.

*(Fitowa 36.35-38)*

31 “Ka yi labule mai ruwan shuɗi, shunayya da jan zare da kuma lallausan lilin da
aka tuƙa, da zānen kerubobin da mai fasaha ya yi. 32 Ka rataye shi a bisa dogayen
sanduna huɗun nan na itacen ƙirya, waɗanda aka dalaye da zinariya, waɗanda suke
tsaya a rammuka huɗu na azurfa. 33 Ka rataye labule daga maɗauri, ka sa akwatin
alkawari a bayan labulen. Labulen zai raba Wurin Mai Tsarki da Wurin Mafi Tsarki.
34 Ka sa murfin kafara a bisa akwatin alkawari a Wuri Mafi Tsarki. 35 Ka sa tebur a
gaba labulen, a gefen arewa na tabanakul, ka kuma sa wurin ajiye fitilan ɗaura da
shi, a wajen kudu.
36 “Game da ƙofar shigar tenti kuwa, ka yi labule mai ruwan shuɗi, shunayya da
jan zare na lallausan lilin da aka tuƙa, aikin gwani. 37 Ka yi ƙugiyoyin zinariya domin
wannan labule da katakai itacen ƙirya biyar, waɗanda aka dalaye da zinariya. Ka
kuma yi zubi na tagulla biyar dominsu.

# 27

## *Bagaden hadaya ta ƙonawa*

*(Fitowa 38.1-7)*

1 “Ka gina bagade da itacen ƙirya, mai tsawo kamu uku, zai zama murabba'i, mai
tsawo kamu biyar, fāɗi kuma kamu biyar. 2 Ka yi masa ƙaho a kowace kusurwan
nan huɗu, domin bagade da ƙahoni duk su zama ɗaya, ka dalaye bagade da tagulla.
3 Ka yi duk kayan aikinsa da tagulla, tukwanensa na ɗiban toka, da manyan cokula,
da kwanonin yayyafawa, da cokula masu yatsotsi don nama da kuma farantai domin
wuta. 4 Ka yi raga na tagulla dominsa, ka kuma yi zoben tagulla a kowace kusurwan
nan huɗu na bagaden. 5 Ka sa ragar a ƙarƙashin bagade domin tă kai tsakiyar bagade.
6 Ka yi wa bagaden sanduna da itacen ƙirya, ka dalaye su da tagulla. 7 Za a zura
sandunan a cikin zoban saboda su kasance a gefe biyu na bagade a lokacin da ake
ɗaukarsa. 8 Ka yi bagaden da katakai, sa'an nan ka robe cikinsa. Ka yi shi bisa ga
fasalin da aka nuna maka a bisa dutsen.

## *Filin tabanakul*

*(Fitowa 38.9-20)*

9 “Ka yi fili domin tabanakul. Tsawon gefen kudu zai zama kamu ɗari da labulen
da aka yi da zaren lili mai kyau, 10 da katakai ashirin da rammukan tagulla ashirin da
ƙugiyoyin azurfa da kuma rammuka a kan katakai. 11 A wajen arewa shi ma, tsawon
yă zama ƙafa ɗari. Ka kama labulen da ƙugiyoyin da aka yi da azurfa waɗanda aka
manna a kan ƙarfen da aka dalaye da azurfa.
12 “Faɗin ƙarshen filin a yamma zai zama kamu hamsin. A kuma sa labule tare da
rammuka goma da kuma katakai goma. 13 A wajen gabas can ƙarshe, wajen fitowar
rana, fāɗin filin zai zama kamu hamsin. 14 Tsayin labulen ƙofa na gefe ɗaya zai
zama kamu goma sha biyar, da katakai uku tare da rammukansu uku, 15 haka kuma
tsayin labule na wancan gefen, zai zama kamu goma sha biyar, da katakai uku tare
da rammukansu uku.
16 “Domin ƙofar tentin, a saƙa labule mai tsayin kamu ashirin da lallausan zaren
lilin mai ruwan shuɗi, da shunayya, da jan zare, mai aikin gwani, da katakai huɗu

tare da rammukansu huɗu. 17 Duk katakan da suke kewaye da filin, za a yi musu
maɗaurai na azurfa da kuma ƙugiyoyi, da rammukan tagulla. 18 Tsayin filin zai zama
kamu ɗari, fāɗinsa kuma kamu hamsin, tsayin labulensa na lallausan zaren lilin zai
zama kamu biyar, a kuma yi rammukansa da tagulla. 19 Dukan sauran kayan da aka
yi amfani da su a aikin wannan tabanakul, ko da wanda irin aiki ne za a yi da su,
har da dukan dogayen turakunsa da na filin, za a yi su da tagulla ne.

### *Mai don wurin ajiye fitila*
### *(Firistoci 24.1-4)*

20 “Ka umarci Isra’ilawa su kawo tsabtataccen mai, tatacce daga zaitun domin fitilu,
saboda fitilun su yi ta ci a koyaushe. 21 A cikin Tentin Sujada, a waje da labulen da
yake a gaban Akwatin Alkawari, Haruna da ’ya’yansa za su sa fitilu su yi ta ci a gaban
UBANGIJI, daga yamma har safiya. Wannan za tă zama dawwammamiyar farilla a
cikin Isra’ila har tsararraki masu zuwa.

# 28

### *Rigunan firistoci*
### *(Fitowa 39.1-7)*

1 “Ka sa a kawo maka Haruna ɗan’uwanka, tare da ’ya’yansa Nadab da Abihu,
Eleyazar da Itamar daga cikin Isra’ilawa, domin su yi mini hidima a matsayin firistoci.
2 Ka yi tufafi masu tsarki domin ɗan’uwanka Haruna, domin a girmama, a kuma
ɗaukaka shi. 3 Ka faɗa wa dukan gwanayen da na ba su hikima a irin abubuwan
nan, cewa su yi tufafi saboda Haruna, don a tsarkakewarsa, domin yă yi mini hidima
a matsayin firist. 4 Waɗannan su ne tufafin da za su ɗinka, ƙyallen maƙalawa a
ƙirji, da efod, da taguwa, da doguwar riga, da rawani, da abin ɗamara. Za su yi wa
ɗan’uwanka, Haruna da ’ya’yansa, waɗannan tsarkaka tufafi, don su zama firistoci
masu yi mini hidima. 5 Ka sa su yi amfani da zinariya, da zare mai ruwan shuɗi da
shunayya da ja, da kuma lallausan lilin.

### *Efod*
### *(Fitowa 39.2-7)*

6 “Ka yi efod da zinariya, da shuɗi, da shunayya, da jan zare, da kuma lallausan
lilin, aikin gwani mai sana’a. 7 Za a yi fele biyu, gaba da baya, sa’an nan a haɗa, a
ɗinka a mahaɗinsu a kafaɗa. 8 Za a yi mata abin ɗamara da irin kayan da aka yi
efod da shi, wato, da zinariya, da shuɗi, da shunayya, da mulufi, da lallausan zaren
lilin.
9 “Ka ɗauki duwatsu biyu masu daraja, ka rubuta sunayen ’ya’yan Isra’ila a kai
10 bisa ga haihuwarsu, sunaye shida a kan dutse ɗaya, saura shida kuma a kan ɗaya
dutsen. 11 A rubuta sunayen ’ya’yan Isra’ila a kan duwatsu biyun, yadda mai yin aiki
da dutse mai daraja yakan zāna hatimi. Sa’an nan a sa kowane dutse a cikin tsaiko na
zinariya 12 a ɗaura su a kan ƙyallen kafaɗa efod a matsayin duwatsun tuni ga ’ya’yan
Isra’ila. Haruna ne zai ɗauki sunayen a kafaɗarsa don tuni a gaban UBANGIJI. 13 Ka
yi tsaiko na zinariya 14 da tuƙaƙƙun sarƙoƙi biyu kamar igiya, na zinariya zalla, ka
kuma ɗaura wa tsaikunan nan biyu tuƙaƙƙun sarƙoƙi.

### *Kyallen maƙalawa a ƙirji*
### *(Fitowa 39.8-21)*

15 “Ka shirya ƙyallen da za a manna a ƙirji don neman nufin Allah. Sai a saƙa shi
da gwaninta kamar yadda aka saƙa efod ɗin. A saƙa shi da zinariya, da shuɗi, da
shunayya, da mulufi, da lallausan zaren lilin. 16 Zai zama murabba’i, tsawonsa kamu
ɗaya, fāɗinsa kuma kamu ɗaya, a naɗe shi biyu. 17 Sa’an nan ka yi jeri huɗu na
duwatsu masu daraja a kansa. A jeri na fari, a sa yakutu, da tofaz, da zumurrudu.

18 A jeri na biyu, a sa turkuwoyis, da saffaya, da emeral. 19 A jeri na uku, a sa yakin,
da idon mage da ametis. 20 A jeri na huɗu, a sa kirisolit, da onis, da yasfa. Ka sa
su a tsaiko na zinariya. 21 A bisa duwatsun nan goma sha biyu, sai a zāna sunayen
ʼyaʼyan Israʼila bisa ga kabilansu goma sha biyu. Za a zāna sunayen kamar hatimi.

22 “Ka yi wa ƙyallen maƙalawa a ƙirjin tuƙaƙƙun sarƙoƙin zinariya zalla. 23 Ka
yi zobe biyu na zinariya saboda ƙyallen maƙalawa a ƙirjin, ka kuma ɗaura su a
kusurwoyin ƙyallen maƙalawa a ƙirji. 24 Ka ɗaura sarƙoƙin zinariyan nan biyu a
zoban a kusurwan ƙyallen maƙalawa a ƙirji. 25 Ka kuma sa sauran bakunan sarƙoƙin
nan biyu a kan tsaikon nan biyu, kana haɗa su da ƙyallen kafaɗa na efod a gaba.
26 Ka yi zobai biyu na zinariya ka ɗaura su ga sauran kusurwoyi ƙyallen maƙalawa
a ƙirji, a gefen ciki kusa da efod. 27 Ka ƙara zobai biyu, ka kuma ɗaura su a bakin
ƙyallen da ya sauka daga kafaɗa ta gaban efod, kusa da mahaɗin ƙyallaye biyu a
bisa ɗamara na efod. 28 Za a ɗaura zoban ƙyallen maƙalawa a ƙirji a zoban efod da
shuɗiyar igiya, domin ƙyallen maƙalawa a ƙirji yă zauna a bisa abin ɗamarar efod,
don kada yă kunce.

29 “Duk saʼad da Haruna zai shiga Wuri Mai Tsarki, zai shiga riƙe da sunayen
ʼyaʼyan Israʼila a zuciyarsa a kan ƙyallen maƙalawa a ƙirji na neman nufin Allah,
domin yă zama abin tunawa a gaban Ubangiji. 30 Ka kuma sa Urim da Tummim
a ƙyallen maƙalawa a ƙirji, don su kasance a zuciyar Haruna, a duk saʼad da zai
shiga gaban Ubangiji. Haka kuwa kullum Haruna zai riƙa kai koke-koken Israʼilawa
a gaban Ubangiji.

### *Sauran rigunan firistoci*
### *(Fitowa 39.22-26,30,31)*

31 “Ka yi taguwar efod da shuɗi duka, 32 ka yanke wuya a tsakiyarta don sawa.
A kuma naɗe wuyan rigar yă yi kauri domin kada yă yage. 33 Za a yi wa bakin
rigar ado da fasalin ʼyaʼyan rumman masu launin shuɗi, da shunayya, da mulufi. A
sa ƙararrawa ta zinariya a tsakankaninsu. 34 Za ka jera su bi da bi, wato, ʼyaʼyan
rumman na biye da ƙararrawar zinariya kewaye da bakin rigar. 35 Dole Haruna yă
sa shi saʼad da yake hidima. Za a ji ƙarar ƙararrawar saʼad da zai shiga Wuri Mai
Tsarki a gaban Ubangiji, da saʼad da ya fita, don kada yă mutu.

36 “Ka yi allo na zinariya zalla, ka kuma yi rubutu a kansa kamar na hatimi, haka,

Mai tsarki ga Ubangiji.

37 Ka ɗaura shi da igiyar ruwa bula domin a haɗa shi da rawani; zai kasance a gaban
rawanin. 38 Zai kasance a goshin Haruna, ta haka zai ɗauki kurakuran da ya yiwu
Israʼilawa sun yi cikin miƙa baye-bayensu masu tsarki. Zai kasance a goshin Haruna
kullayaumin, domin su zama abin karɓa ga Ubangiji.

39 “Ka saƙa doguwar riga da lallausan lilin ka kuma yi hula da lallausan zaren lilin,
ka kuma saƙa abin ɗamara mai ado.

*(Fitowa 39.27-29)*

40 “Ka saƙa doguwar riga, abin ɗamara da kuma huluna domin ʼyaʼyan Haruna,
don yă ba su girma da ɗaukaka. 41 Bayan ka sa waɗannan riguna wa ɗanʼuwanka
Haruna da ʼyaʼyansa, ka shafe su da mai, ka kuma naɗa su. Ka keɓe su domin su yi
mini hidima a matsayin firistoci.

42 “Ka yi ʼyan wandunan ciki na lilin don su rufe tsiraicinsu, tsayinsu zai kama daga
kwankwaso zuwa cinya. 43 Dole Haruna da ʼyaʼyansa su sa su saʼad da za su shiga
Tentin Sujada, ko saʼad da suka kusace bagade domin hidima a Wuri Mai Tsarki, don
kada su yi laifi, su kuma mutu.

“Wannan za tă zama dawwammamiyar farilla wa Haruna da zuriyarsa har abada.

# 29

*Keɓewar firistoci*
*(Firistoci 8.1-36)*

1 “Ga abin da za ka yi don ka keɓe su, don su yi mini hidima a matsayin firistoci.
Ka ɗauki ɗan bijimi da raguna biyu marasa lahani. 2 Daga garin alkama mai laushi
marar yisti kuwa, ka yi burodi, da wainan da aka kwaɓa da mai, da ƙosai waɗanda
an barbaɗa mai a kai. 3 Ka sa waɗannan a cikin kwando. Sa’an nan ka miƙa su tare
da ɗan bijimin da ragunan nan biyu. 4 Bayan haka sai ka kawo Haruna da ’ya’yansa
a ƙofar Tentin Sujada ka yi musu wanka. 5 Ka ɗauki rigar ka sa wa Haruna, ka sa
masa doguwar rigar, da rigar efod, da efod kanta, da ƙyallen maƙalawa a ƙirji. Ka
ɗaura masa efod da ɗamarar da aka yi mata ado. 6 Ka naɗa masa rawani a kai, ka
kuma sa kambi mai tsarki a bisa rawanin. 7 Ka ɗauki man shafewa ka shafe shi, ta
wurin zuba man a kansa. 8 Ka kawo ’ya’yansa, ka sa musu taguwoyi, 9 ka kuma sa
musu huluna a kansu. Sa’an nan ka ɗaura wa Haruna da ’ya’yansa abin ɗamara.
Su kuwa da zuriyarsu, aikin firist kuwa zai zama nasu ta wurin dawwammamiyar
farilla.

“Ta haka za ka keɓe Haruna da ’ya’yansa maza.

10 “Ka kuma kawo bijimin a gaban Tentin Sujada, sai Haruna da ’ya’yansa su ɗora
hannuwansu a kansa. 11 Ka yanka shi a gaban Ubangiji a ƙofar Tentin Sujada. 12 Ka
ɗibi jinin bijimin ka zuba a kan ƙahoni na bagade da yatsanka, sauran jinin kuwa ka
zuba a gindin bagaden. 13 Sa’an nan ka ɗauki dukan kitsen da ya rufe kayan ciki, da
kitsen da yake manne da hanta, da ƙoda biyu da kuma kintsen da yake a kansu, ka
ƙone su a kan bagade. 14 Amma ka ƙone naman bijimin, da fatarsa, da kayan cikin,
a bayan sansani. Hadaya ce ta zunubi.

15 “Ka ɗauki ɗaya daga cikin ragunan, Haruna kuwa da ’ya’yan maza za su ɗora
hannuwansa a kansa. 16 Ka yanka ragon, ka ɗibi jinin, ka yayyafa shi kewaye da
gefen bagaden. 17 Ka yayyanka rago gunduwa-gunduwa, ka wanke kayan cikin, da
ƙafafun, da kan, ka haɗa su da gunduwoyin. 18 Sa’an nan ka ƙone ragon ɗungum a
kan bagade. Hadaya ta ƙonawa ce ga Ubangiji, mai daɗin ƙanshi, wato, hadaya ce
da aka ƙone da wuta ga Ubangiji.

19 “Ka ɗauki ɗayan ragon, sai Haruna da ’ya’yansa maza su ɗora hannuwansu a
kansa. 20 Ka yanka ragon, ka ɗibi jinin, ka shafa a bisa leɓen kunnen Haruna na
dama, da bisa leɓen kunnuwan ’ya’yansa maza na dama, da kan manyan yatsotsin
hannuwansu na dama, da kuma a kan manyan yatsotsin ƙafafunsu na dama. Sauran
jinin kuwa, sai ka yayyafa shi kewaye da gefen bagaden. 21 Ka ɗibi jinin da yake a
kan bagade, da man shafewa, ka yafa a kan Haruna da rigunansa, da kuma a kan
’ya’yansa maza da rigunansu. Sa’an nan shi da ’ya’yansa maza da rigunansu za su
tsarkake.

22 “Ka ɗebi kitse daga wannan rago, ka yanke wutsiyarsa mai kitse, ka kuma ɗebi
kitsen da ya rufe kayan ciki, da kitsen da yake bisa hanta, da ƙoda biyu da kitsen
da yake kansu, da cinyar dama. (Gama rago ne don naɗi.) 23 Daga kwandon burodi
marar yisti, wanda yake gaban Ubangiji, ka ɗauki dunƙule ɗaya, da waina da aka yi
da mai, da kuma ƙosai. 24 Ka sa dukan waɗannan a hannun Haruna da ’ya’yansa
maza, su kaɗa su a gaban Ubangiji a matsayin hadaya ta kaɗawa. 25 Sa’an nan
ka karɓe su daga hannuwansu, ka ƙone su a kan bagade tare da hadaya ta ƙonawa,
domin ƙanshi mai daɗi ga Ubangiji, wato, hadaya ce da aka ƙone da wuta ga Ubangiji.
26 Bayan haka, ka ɗauki ƙirjin ragon domin naɗin Haruna, ka kaɗa shi a gaban
Ubangiji kamar hadaya ta kaɗawa. Wannan ƙirji zai zama rabonka.

27 “Ka tsarkake ƙirji na hadaya ta kaɗawa, da cinya ta hadaya ta ɗagawa, waɗanda
za a kaɗa a kuma ɗaga na ragon naɗin, wanda yake na Haruna da kuma na ’ya’yansa

maza. 28 Wannan zai zama rabon Haruna da ʼyaʼyansa maza daga Israʼilawa. Gama
wannan hadaya ta ɗagawa ce daga cikin hadayu na salama da Israʼilawa za su miƙa
wa Ubangiji.
29 “Keɓaɓɓun tufafin nan na Haruna za su zama na zuriyarsa bayan mutuwarsa.
Da tufafin nan ne za a zuba musu mai, a keɓe su. 30 Ɗan da ya gāje shi a matsayin
firist, shi ne zai sa su har kwana bakwai, lokacin da ya shiga Tentin Sujada, don yă
yi aiki a Wuri Mai Tsarki.
31 “Ka ɗauki ragon naɗi, ka dafa naman a tsattsarkan wuri. 32 A ƙofar Tentin
Sujada, Haruna da ʼyaʼyansa maza za su ci wannan rago da burodin da yake cikin
kwandon. 33 Za su ci abubuwan nan da aka yi kafara da su a lokacin tsarkakewarsu
da keɓewarsu. Ba wanda zai ci, sai su kaɗai, gama abubuwan nan tsarkaka ne. 34 In
naman ragon naɗi ko wani burodin ya ragu har safiya, a ƙone shi, kada a ci gama
tsarkake ne.
35 “Ka yi wa Haruna da ʼyaʼyansa maza duk abin da na umarce ka, ka ɗauki kwana
bakwai don naɗinsu. 36 Ka miƙa bijimi ɗaya kowace rana domin hadaya don zunubi
ta yin kafara. Ka tsarkake bagade ta wuri yin kafara dominsa, ka shafe shi da mai don
ka tsarkake shi. 37 Kwana bakwai za ka yi kafara saboda bagaden, ka kuma tsarkake
shi. Saʼan nan bagaden zai zama mafi tsarki, kuma duk abin da ya taɓa bagaden zai
tsarkaka.

*(Firistoci 6.8-13; Kidaya 28.1-8)*

38 “Ga abin da za ka miƙa a bisa bagaden kowace rana. ʼYan raguna biyu masu
shekara ɗaya-ɗaya. 39 Ka miƙa ɗaya da safe, ɗaya kuma da yamma. 40 Haɗe da ɗan
rago na farkon, ka miƙa mudun gari mai laushi wanda an gauraye da kwalaba ɗaya
na tataccen mai zaitun, da kwalaba ɗaya na ruwan inabi don hadaya ta sha. 41 Ka
miƙa ɗaya ragon da yamma, tare da hadaya ta gari da hadaya ta sha kamar aka yi
ta safe, mai daɗin ƙanshi, wato, hadaya ce da aka ƙone da wuta ga Ubangiji.
42 “Wannan za tă zama hadaya ta ƙonawar da za a dinga yi kowace rana, daga
tsara zuwa tsara. Za a yi ta miƙa hadayar a ƙofar Tentin Sujada a gaban Ubangiji. A
can zan sadu da kai, in yi magana da kai; 43 a can kuma zan sadu da Israʼilawa, in
kuma tsarkake wurin da ɗaukakata.
44 “Ta haka zan tsarkake Tentin Sujada da bagaden, in kuma tsarkake Haruna da
ʼyaʼyansa maza su yi mini hidima a matsayin firistoci. 45 Saʼan nan zan zauna a cikin
Israʼilawa, in kuma zama Allahnsu. 46 Za su san cewa ni ne Ubangiji Allahnsu, wanda
ya fitar da su daga Masar saboda in zauna a cikinsu. Ni ne Ubangiji Allahnsu.

# 30

*Bagaden turare*
*(Fitowa 37.25-28)*

1 “Ka yi bagade da itacen ƙirya don ƙona turare. 2 Zai zama murabbaʼi, tsawon zai
zama kamu ɗaya, fāɗi kuma kamu ɗaya, amma tsayin yă zama kamu biyu, ƙahoninsa
kuma su zama ɗaya da shi. 3 Ka dalaye bisansa da kuma dukan gefe-gefensa da kuma
ƙahoninsa da zinariya zalla, ka kuma yi zubi na zinariya kewaye da shi. 4 Ka yi zobai
biyu na zinariya domin bagade a ƙarƙashin zubin, biyu a gefe da gefe su fuskanci
juna, don su riƙe sandunan da ake amfani da su don ɗaukarsa. 5 Ka yi sandunan nan
da itacen ƙirya, ka dalaye su da zinariya. 6 Ka sa bagaden a gaban labulen da yake
gaban akwatin alkawari, a gaba murfin kafara wanda yake bisa akwatin alkawari,
inda zan sadu da kai.
7 “Haruna zai ƙone turare a bisa bagaden kowace safiya, saʼad da yake shirya fitilu.
8 Dole Haruna yă ƙone turare saʼad da ya ƙuna fitilu da yamma, ta haka za a riƙa
ƙona turare a gaban Ubangiji, daga tsara zuwa tsara. 9 Ba za a ƙona wani irin turare

dabam a bisa wannan bagade ba, ba kuma za a miƙa hadaya ta ƙonawa, ko ta hatsi,
ko ta sha a bisansa ba. 10 Sau ɗaya a shekara, Haruna zai yi kafara a bisa ƙahoninsa.
Dole a yi wannan kafara ta shekara-shekara da jinin kafara ta hadaya don zunubi
daga tsara zuwa tsara. Gama bagaden mafi tsarki ne ga Ubangiji."

*Kuɗin kafara*

11 Sa'an nan Ubangiji ya ce wa Musa, 12 "Sa'ad da za ku ƙidaya Isra'ilawa, dole
kowanne yă biya domin yă fanshe kansa ga Ubangiji a lokacin da aka ƙidaya shi. Ta
haka ɓabu wata annobar da za tă buge su sa'ad da kuke ƙidaya su. 13 Kowannen da
ya ƙetare zuwa wurin waɗanda aka riga aka ƙidaya, dole yă ba da rabin shekel,
bisa ga ma'aunin shekel na tsattsarkan wuri, wanda nauyinsa garwa ashirin ne.
Wannan rabin shekel hadaya ce ga Ubangiji. 14 Duk waɗanda suka ƙetare, waɗanda
shekarunsu ya kai ashirin ko fiye, za su ba da hadaya ga Ubangiji. 15 Masu arziki ba
za su bayar fiye da rabin shekel ba, talakawa kuma ba za su bayar ƙasa da haka ba,
sa'ad da za ku yi hadaya ga Ubangiji don kafara rayukanku. 16 Ku karɓi kuɗin kafara
daga hannun Isra'ilawa, ku yi amfani da shi domin hidimar Tentin Sujada. Zai zama
abin tunawa ga Isra'ilawa a gaban Ubangiji, don su yi kafarar rayukansu."

*Kwano don wanki*
*(Fitowa 38.8)*

17 Sa'an nan Ubangiji ya ce wa Musa, 18 "Ka yi daro na tagulla, ka yi masa ƙafafun
da za a ajiye shi da tagulla don wanki. Ka ajiye shi tsakanin Tentin Sujada da bagade,
ka zuba ruwa a ciki. 19 Haruna da 'ya'yansa maza za su wanke hannuwansu da
ƙafafunsu da ruwan da yake cikinsa. 20 Duk lokacin da suka shiga Tentin Sujada, za
su yi wanka, don kada su mutu. Duk lokacin da suka yi kusa da bagade don hidima
ta miƙa hadayar da aka yi wa Ubangiji da wuta, 21 za su wanke hannuwansu da
ƙafafunsu, don kada su mutu. Wannan za tă zama dawwammamiyar farilla domin
Haruna da zuriyarsa daga tsara zuwa tsara."

*Man shafewa*
*(Fitowa 37.29)*

22 Sa'an nan Ubangiji ya ce wa Musa, 23 "Ka ɗauki waɗannan kayan yaji masu
kyau, shekel 500 na ruwan mur, rabin turaren sinnamon mai daɗin ƙanshi shekel
250, shekel 250 na turaren wuta mai ƙanshi, 24 shekel 500 na kashiya, duk bisa ga
ma'aunin shekel na tsattsarkan wuri, da moɗa na man zaitun. 25 Da waɗannan za
ka yi man shafewa mai tsarki, yadda mai yin turare yake yi. Zai zama man shafewa
mai tsarki. 26 Sa'an nan ka yi amfani da shi don shafa wa Tentin Sujada, da akwatin
alkawari, 27 da tebur da kuma dukan kayansa, da wurin ajiye fitila da dukan kayansa,
da bagaden ƙona turare, 28 bagaden hadaya ta ƙonawa da dukan kayansa, da daro
da mazauninsa. 29 Za ka tsarkake su don su zama mafi tsarki, kuma duk abin da ya
taɓa su, zai zama mai tsarki.
30 "Ka shafe Haruna da 'ya'yansa maza, ka kuma tsarkake su don su yi mini hidima
a matsayin firistoci. 31 Ka faɗa wa Isra'ilawa, 'Wannan mai, zai zama mai tsarki ne a
gare ni don shafewa, daga tsara zuwa tsara. 32 Kada a zuba a jikunan mutane, kada
kuma a yi wani mai irinsa. Wannan mai, mai tsarki ne, za ku kuma ɗauke shi a
matsayi mai tsarki. 33 Duk wanda ya yi irin wannan mai, duk wanda kuma ya shafa
shi a kan wani wanda yake ba firist ba, za a ware shi daga mutanensa.' "

*Turare*

34 Sa'an nan Ubangiji ya ce wa Musa, "Ka ɗauki kayan yaji mai ƙanshi, resin
na gum, da onika, da galbanum, da kuma zallan lubban, duk nauyinsu yă zama
daidai. 35 Ka yi turare mai ƙanshi yadda mai yin turare yake yi. A sa masa gishiri, yă
zama tsabtatacce, tsarkakakke. 36 Ka ɗiba kaɗan daga ciki, ka niƙa, ka ajiye a gaban

akwatin alkawari a cikin Tentin Sujada, inda zan sadu da kai. Zai zama mafi tsarki
a gare ku. 37 Kada ku yi wani turare irinsa wa kanku; ku ɗauke shi a matsayi mai
tsarki ga UBANGIJI. 38 Duk wanda ya yi irinsa don jin daɗin ƙanshinsa, dole a ware
shi daga mutanensa.”

# 31

*Bezalel da Oholiyab*
*(Fitowa 35.30–36.1)*

1 Sai UBANGIJI ya ce wa Musa, 2 “Duba, na zaɓi Bezalel ɗan Uri, ɗan Hur, na kabilar
Yahuda, 3 na kuma cika shi da Ruhun Allah, fasaha, azanci, da kuma sani cikin kowace
irin sana’a, 4 don yin zāne-zāne na aikin zinariya, azurfa da tagulla, 5 don yanka da
shirya duwatsu, yin aikin katako, da kuma yin kowane irin aikin sana’ar hannu.
6 Ban da haka, na zaɓi Oholiyab ɗan Ahisamak, na kabilar Dan, don yă taimake shi.
Na kuma ba da fasaha ga dukan masu aikin sana’ar hannu, don yin duk abin da na
umarce ka. 7 Tentin Sujada, akwatin Alkawari tare da murfin kafara a bisansa, da
dukan kayan aiki na tentin, 8 tebur da kayansa, wurin ajiye fitila na zinariya zalla, da
dukan kayansa, bagaden ƙona turare, 9 bagaden hadaya ta ƙonawa da dukan kayansa,
daro tare da mazauninsa, 10 da kuma saƙaƙƙun riguna, tsarkakan riguna don Haruna
firist da rigunan ’ya’yansa maza, sa’ad da suke hidima a matsayin firistoci, 11 da man
shafewa, da turare mai ƙanshi don Wuri Mai Tsarki. Za a yi su kamar yadda na
umarce ka.”

*Asabbaci*

12 Sa’an nan UBANGIJI ya ce wa Musa, 13 “Ka faɗa wa Isra’ilawa, ‘Dole ku kiyaye
Asabbataina. Wannan zai zama alama tsakanina da ku daga tsara zuwa tsara, saboda
ku sani ni ne UBANGIJI, wanda ya mai da ku masu tsarki.

14 “ ‘Ku kiyaye Asabbaci, domin yă zama mai tsarki a gare ku. Duk wanda ya
ƙazantar da shi, za a kashe shi; duk wanda ya yi wani aiki a ranar, za a ware shi
daga mutane. 15 Kwana shida, za a yi aiki, amma a rana ta bakwai, Asabbaci ne na
hutu, mai tsarki ga UBANGIJI. Duk wanda ya yi wani aiki a Asabbaci, za a kashe shi.
16 Isra’ilawa za su kiyaye Asabbaci, suna bikinsa daga tsara zuwa tsara a matsayin
madawwamin alkawari. 17 Zai zama alama tsakanina da Isra’ilawa har abada, gama
cikin kwana shida UBANGIJI ya yi sama da ƙasa, a rana ta bakwai kuma ya daina aiki,
ya kuma huta.’ ”

18 Sa’ad da UBANGIJI ya gama yin wa Musa magana a kan Dutsen Sinai, sai ya ba
shi alluna biyu na Alkawari, allunan duwatsu rubutattu da yatsan Allah.

# 32

*Ɗan maraƙin zinariya*
*(Maimaitawar Shari’a 9.6-29)*

1 Sa’ad da mutane suka ga Musa ya daɗe bai sauko daga dutse ba, sai suka taru
kewaye da Haruna suka ce, “Zo, ka yi mana alloli waɗanda za su yi mana jagora.
Game da wannan Musa wanda ya fitar da mu daga Masar dai, ba mu san abin da ya
faru da shi ba.”

2 Haruna ya amsa musu ya ce, “Ku tuttuɓe zoban zinariya waɗanda suke kunnuwan
matanku, da na ’ya’yanku maza da mata, ku kawo mini.” 3 Saboda haka dukan
mutane suka tuttuɓe ’yan kunnensu suka kawo wa Haruna. 4 Sai ya karɓi abubuwan
da suka ba shi, ya yi gunki na siffar ɗan maraƙi, ya sassaƙa shi da kayan aiki. Sa’ad
da mutane suka gani, sai suka tā da murya suka ce, “Waɗannan su ne allolinku, ya
Isra’ila, waɗanda suka fitar da ku daga Masar.”

5 Da Haruna ya ga haka, sai ya gina bagade a gaban ɗan maraƙi, ya yi shela ya
ce, "Gobe akwai biki ga UBANGIJI." 6 Saboda haka kashegari, mutane suka tashi da
sassafe suka miƙa hadaya ta ƙonawa, da hadaya ta salama. Bayan haka suka zauna
suka ci, suka sha, suka kuma tashi suka yi rawa.
7 Sai UBANGIJI ya ce wa Musa, "Sauka, gama mutanenka, waɗanda ka fitar da su
daga Masar sun ƙazantu. 8 Sun yi saurin juyawa daga abin da na umarce su, sun
kuma yi wa kansu gunki na siffar ɗan maraƙi. Sun yi sujada ga ɗan maraƙi, suka yi
hadaya gare shi, suka kuma ce, waɗannan su ne allolinka ya Isra'ila, waɗanda suka
fito da kai daga Masar."
9 UBANGIJI ya ce wa Musa, "Na ga waɗannan mutane, mutane ne masu taurinkai."
10 Yanzu ka bar ni kurum fushina yă yi ƙuna a kansu, in hallaka su. Sa'an nan in
maishe ka al'umma mai girma.
11 Amma Musa ya nemi tagomashin UBANGIJI, Allahnsa ya ce, "Ya UBANGIJI don me
fushinka zai yi ƙuna a kan mutanenka, waɗanda ka fisshe su daga Masar da ikon
hannunka mai girma? 12 Don me za ka sa Masarawa su ce, 'Ai, da mugun nufi ne ya
fito da su don yă shafe su daga fuskar duniya'? Ka juya daga fushinka mai zafi, ka
ji tausayi, kada ka kawo masifa a kan mutanenka. 13 Ka tuna da bayinka Ibrahim,
Ishaku da Isra'ila, waɗanda ka rantse da kanka cewa, 'Zan mai da zuriyarka kamar
taurarin sama kuma zan ba wa zuriyarka wannan ƙasa wadda na yi musu alkawari,
za tă kuma zama abin gādonsu har abada.' " 14 Sai UBANGIJI ya yi juyayi, bai kuwa
kawo wa mutanensa bala'in da ya yi niyya ba.
15 Musa ya juya, ya sauka daga kan dutsen da alluna biyu na Alkawari a
hannuwansa. An yi rubutun a kowane gefe, gaba da baya. 16 Allunan aikin Allah
ne; rubutun kuma rubutun Allah ne, da ya zāna a kan alluna.
17 Sa'ad da Yoshuwa ya ji surutun mutane suna ihu, sai ya ce wa Musa, "Kamar
akwai ƙarar yaƙi a sansani."
18 Musa ya amsa ya ce,
"Ba ƙarar nasara ba ce,
ba ƙarar wanda yaƙi ya ci ba ne;
ƙarar waƙa ce nake ji."
19 Da Musa ya kusato sansanin, sai ya ga ɗan maraƙin da kuma mutane suna rawa.
Sai fushinsa ya yi ƙuna, ya kuwa jefar da allunan da suke hannuwansa, allunan kuwa
suka farfashe a gindin dutsen. 20 Sai ya ɗauki ɗan maraƙin da suka yi, ya ƙone a
wuta; sa'an nan ya niƙa shi ya zama gari, ya barbaɗa garin a ruwa, ya sa Isra'ilawa
suka sha.
21 Ya ce wa Haruna, "Mene ne waɗannan mutane suka yi maka da ka kai su ga
wannan zunubi mai girma?"
22 Haruna ya amsa ya ce, "Kada ka yi fushi da ni ranka yă daɗe, ka san yadda
mutanen nan suke da saurin yin mugunta. 23 Sun ce mini, 'Ka yi mana alloli waɗanda
za su yi mana jagora, game da wannan Musa dai, wanda ya fito da mu daga Masar,
ba mu san abin da ya faru da shi ba.' 24 Sai na gaya musu, 'Duk wanda yana da
kayan ado na zinariya, ya cire?' Sa'an nan suka ba ni zinariya, sai na jefa cikin wuta,
wannan ɗan maraƙi ya fito."
25 Musa ya duba ya ga mutane sun kauce gaba ɗaya domin Haruna ya sa suka kauce,
har suka zama abin dariya ga abokan gābansu. 26 Saboda haka sai ya tsaya a ƙofar
sansani ya ce, "Duk wanda yake na UBANGIJI yă zo wurina." Sai dukan Lawiyawa
suka taru wurinsa.
27 Sa'an nan ya ce musu, "Ga abin da UBANGIJI, Allah na Isra'ila ya ce, 'Kowane
mutum yă rataya takobinsa, yă kai yă kawo daga wannan gefe zuwa wancan
cikin sansani, kowa yă kashe ɗan'uwansa, da abokinsa, da kuma maƙwabcinsa.' "

28 Lawiyawa suka yi yadda Musa ya umarta, a ranar, mutane wajen dubu uku suka
mutu. 29 Sa'an nan Musa ya ce, "An keɓe ku ga UBANGIJI a yau, gama kun yi gāba da
'ya'yanku da 'yan'uwanku, ya kuma albarkace ku a wannan rana."
30 Kashegari Musa ya ce wa mutane, "Kun yi zunubi mai girma. Amma yanzu zan
hau wurin UBANGIJI; wataƙila zan iya yin kafara domin zunubinku."
31 Don haka Musa ya koma wurin UBANGIJI ya ce, "Kaito, mutanen nan sun yi zunubi
mai girma! Sun yi wa kansu allolin zinariya. 32 Amma yanzu, ina roƙonka ka gafarta
zunubinsu, in ba haka ba, to, ka shafe ni daga littafin da ka rubuta."
33 UBANGIJI ya amsa wa Musa, "Duk wanda ya yi mini zunubi, shi zan shafe daga
littafina. 34 Yanzu tafi, ka jagoranci mutanen zuwa inda na yi zance, mala'ikana kuma
zai sha gabanku. Duk da haka sa'ad da lokaci ya yi da zan yi horo, zan hore su domin
zunubinsu."
35 UBANGIJI kuwa ya bugi mutanen da annoba, saboda abin da suka yi da ɗan
maraƙin da Haruna ya yi.

# 33

1 Sa'an nan UBANGIJI ya ce wa Musa, "Ka bar wannan wuri, kai da mutanen da ka
fito da su daga Masar, ka haura zuwa ƙasar da na alkawarta da rantsuwa wa Ibrahim,
Ishaku da Yaƙub cewa, 'Zan ba zuriyarka.' 2 Zan aika da mala'ika a gabanka in kuma
kori Kan'aniyawa, Amoriyawa, Hittiyawa, Ferizziyawa, Hiwiyawa da Yebusiyawa.
3 Ka haura zuwa ƙasar da take zub da madara da zuma. Amma ba zan tafi tare da ku
ba, saboda ku mutane ne masu taurinkai domin mai yiwuwa in hallaka ku a hanya."
4 Da mutane suka ji wannan mugun magana, sai suka fara makoki. Ba kuma wanda
ya sa kayan ado. 5 Gama UBANGIJI ya riga ya ce wa Musa, "Ka faɗa wa Isra'ilawa, 'Ku
mutane ne masu taurinkai. In na yi tafiya da ku ko na ɗan lokaci, mai yiwuwa in
hallaka ku. Yanzu sai ku tuɓe kayan adonku, zan kuwa yanke shawara a kan abin da
zan yi da ku.' " 6 Saboda haka Isra'ilawa suka tuttuɓe kayan adonsu a Dutsen Horeb.

### *Tentin sujada*

7 Musa fa ya saba ɗaukan tenti yă kafa shi a bayan sansani da ɗan nisa, yana
kiransa "Tentin Sujada." Duk wanda yake neman wani abu daga wurin UBANGIJI sai
yă tafi Tentin Sujada a bayan sansani. 8 A sa'ad da kuma Musa ya fita zuwa Tentin,
dukan mutanen sukan tashi su tsaya a ƙofofin tentinsu, suna kallon Musa, sai ya
shiga tentin. 9 Yayinda Musa ya shiga cikin tentin, sai al'amudin girgije yă sauko, yă
tsaya a ƙofar yayinda UBANGIJI yana magana da Musa. 10 Lokacin da mutane suka ga
al'amudin girgije a tsaye a ƙofar tentin, sai duk su miƙe tsaye su yi sujada, kowa a
ƙofar tentinsa. 11 UBANGIJI yakan yi magana da Musa fuska da fuska, kamar yadda
mutum yake magana da abokinsa. Sa'an nan Musa yă koma sansani, amma saurayin
nan Yoshuwa ɗan Nun mai taimakonsa ba ya barin tentin.

### *Musa da ɗaukakar UBANGIJI*

12 Musa ya ce wa UBANGIJI, "Kana ta faɗa mini cewa, 'Ka jagoranci mutane nan,'
amma ba ka faɗa mini wanda zai tafi tare da ni ba. Ga shi ka ƙara ce mini, 'Na san
ka, na san sunanka, ka kuma sami tagomashi a wurina.' 13 In ka ji daɗina, ka koya
mini hanyarka don in san ka, in kuma ci gaba da samun tagomashi daga gare ka. Ka
tuna cewa wannan al'umma mutanenka ne."
14 UBANGIJI ya amsa ya ce, "Zan tafi tare da kai, zan kuma rage maka nauyin kaya."
15 Musa kuwa ya ce masa, "In ba za tă tafi tare da mu ba, to, kada ka ɗaga mu daga
nan. 16 Yaya wani zai sani ko ka ji daɗina da kuma mutanenka, in ba ka tafi tare da
mu ba? Mene ne kuma zai bambanta ni da mutanenka daga sauran jama'ar da suke
a duniya?"

17 Sai UBANGIJI ya ce wa Musa, “Zan yi yadda ka faɗa, gama ka sami tagomashi a
wurina, na san ka, na kuma san sunanka.”
18 Musa kuwa ya ce, “To, ka nuna mini ɗaukakarka.”
19 Sai UBANGIJI ya ce, “Zan wuce a gabanka, Ni UBANGIJI zan yi shelar sunana a
gabanka. Zan yi alheri ga duk wanda na so in yi masa alheri, zan nuna jinƙai ga
duk wanda na so in yi masa jinƙai. 20 Amma ya ce, ba za ka ga fuskata ba, don ba
mutumin da zai gan ni yă rayu.”
21 Sa’an nan UBANGIJI ya ce, “Ga wani wuri kusa da ni inda za ka tsaya bisa dutsen.
22 A sa’ad da ɗaukakata tana wucewa, zan sa ka a cikin tsaguwar dutsen, in rufe ka
da hannuna har sai na wuce. 23 Sa’an nan zan ɗauke hannuna, ka kuwa ga bayana;
amma fuskata, ba za ka gani ba.”

# 34

*Sababbin allunan dutse*
*(Maimaitawar Shari’a 10.1-5)*

1 UBANGIJI ya ce wa Musa “Sassaƙa alluna biyu kamar na farko, ni kuwa in rubuta
kalmomin da suke cikin alluna na farko da ka farfasa. 2 Ka shirya da safe, ka hauro
kan Dutsen Sinai. Ka gabatar da kanka a gare ni a can kan dutse. 3 Ba wani da zai
zo tare da kai, ko a gan shi ko’ina a kan dutsen, kada garkunan tumaki ko na shanu
su yi kiwo kusa da dutsen.”
4 Saboda haka Musa ya sassaƙa alluna biyu na dutse kamar na fari, sai ya hau
Dutsen Sinai da sassafe, kamar yadda UBANGIJI ya umarce shi, yana kuma ɗauke da
alluna biyu na dutse a hannuwansa. 5 Sa’an nan UBANGIJI ya sauko a cikin girgije
ya tsaya can tare da shi, ya kuma yi shelar sunansa. 6 Sai UBANGIJI ya wuce a gaban
Musa, ya yi shela ya ce, “Ni ne UBANGIJI Allah mai tausayi, mai alheri, mai jinkirin
fushi, cike da ƙauna da aminci, 7 nakan nuna ƙauna wa dubbai, nakan kuma gafarta
mugunta, tawaye da zunubi. Amma ba na barin mai laifi, ba tare da na hore shi ba;
nakan hukunta ’ya’ya da jikoki har tsara ta uku da ta huɗu saboda laifin iyaye.”
8 Musa ya yi sauri ya rusuna har ƙasa, ya yi sujada. 9 Ya ce, “Ya Ubangiji, in na
sami tagomashi a idanunka, bari Ubangiji yă tafi tare da mu. Ko da yake wannan
mutane masu taurinkai ne, ka gafarta muguntanmu da zunubanmu, ka kuma sāke
sa mu zama abin gādonka.”

*(Fitowa 23.14-19; Maimaitawar Shari’a 7.1-5; 16.1-17)*

10 Sai UBANGIJI ya ce, “Ga shi na yi alkawari da kai. A gaban dukan mutanenka
zan yi abubuwan banmamakin da ba a taɓa yinsa a cikin wata al’umma a duniya
ba. Mutanen da kuke zaune cikinsu za su ga aikin bantsoro, da Ni UBANGIJI zan yi
muku. 11 Ku yi biyayya da umarnin da na ba ka yau. Zan kora muku Amoriyawa,
Kan’aniyawa, Hittiyawa, Ferizziyawa, Hiwiyawa da Yebusiyawa. 12 Ku kula, kada ku
yi yarjejjeniya da waɗanda suke zaune a ƙasar da za ku tafi, in ba haka ba, za su
zama muku tarko. 13 Ku rurrushe bagadansu, ku farfashe keɓaɓɓun duwatsunsu,
ku sassare ginshiƙan Asheransu.* 14 Kada ku bauta wa wani allah, gama UBANGIJI,
wanda sunansa Kishi, Allah ne mai kishi.
15 “Ku kula, kada ku yi yarjejjeniya da mazaunan wannan ƙasa, don kada sa’ad da
suke yi wa allolinsu sujada, suna miƙa musu hadaya, su gayyace ku, ku ci hadayar da
suka miƙa wa allolinsu. 16 Kada ku auro wa ’ya’yanku maza ’yan matansu, waɗanda
suke yi wa alloli sujada, har su sa ’ya’yanku su bi allolinsu.
17 “Kada ku yi alloli na zubi.

* **34:13** Wato, alamun alliya Ashera

18 “Sai ku yi Bikin Burodi Marar Yisti. Ku kuma ci burodi marar yisti har kwana
bakwai, kamar yadda na umarce ku. Ku yi wannan a ƙayyadadden lokacinsa a watan
Abib, gama a cikin watan ne kuka fita daga Masar.
19 “Dan fari na kowane mutum zai zama nawa, har da ɗan farin na dabbobi, ko
na garken shanu ko na tumaki. 20 Ku fanshi ɗan farin jaki da na tunkiya, amma in
ba ku fanshe shi ba, ku karya wuyansa. Ku fanshi duk ’ya’yan farinku maza.
“Kada wani yă zo gabana hannu wofi.
21 “Kwana shida za ku yi aiki, amma a rana ta bakwai za ku huta; ko da lokacin
noma ne, ko lokacin girbi, sai ku huta.
22 “Ku kiyaye Bikin Makoni wato, bikin girbin nunan fari na alkama, da Bikin Gama
Tattara amfanin gonaki, a ƙarshen shekara. 23 Sau uku a shekara, dukan mazanku
za su bayyana a gaban UBANGIJI Mai Iko Duka, Allah na Isra’ila. 24 Zan kore al’umma
daga gabanku, in fadada kan iyakarku, babu wanda zai yi ƙyashin ƙasarku a lokutan
nan uku na shekara da kuka haura don ku bayyana a gaban UBANGIJI, Allahnku.
25 “Kada ku miƙa mini jinin hadaya tare da wani abin da yana da yisti, kada kuma
ku bar kowace hadaya ta Bikin Ketarewa ta kwana.
26 “Ku kawo nunan farin amfanin gonarku mafi kyau a gidan UBANGIJI, Allahnku.
“Kada ku dafa ɗan akuya a cikin madarar mahaifiyarsa.”
27 Sa’an nan UBANGIJI ya ce wa Musa, “Ka rubuta waɗannan kalmomi, gama bisa
ga kalmomin nan, na yi alkawari da kai da kuma Isra’ila.” 28 Musa ya kasance tare
da UBANGIJI kwana arba’in da dare arba’in, bai ci ba, bai sha ba. Ya kuma rubuta
kalmomin alkawari a kan alluna, wato, dokoki goma.

### *Fuskar Musa mai haske*

29 Sa’ad da Musa ya sauko daga kan Dutsen Sinai tare da alluna biyu na Alkawari
a hannuwansa, bai san cewa fuskarsa tana ƙyalli ba saboda zaman da ya yi a gaban
UBANGIJI. 30 Da Haruna da dukan Isra’ila suka ga Musa, fuskarsa kuma tana ƙyalli,
sai suka ji tsoron zuwa kusa da shi. 31 Amma Musa ya kira su, sai Haruna da dukan
shugabannin jama’ar suka zo wurinsa, ya kuwa yi musu magana. 32 Daga baya sai
dukan Isra’ilawa suka zo kusa da shi, ya kuma ba su dukan dokokin da UBANGIJI ya
ba shi a Dutsen Sinai.
33 Da Musa ya gama magana da su, sai ya lulluɓe fuskarsa. 34 Amma duk sa’ad da
ya je gaban UBANGIJI don yă yi magana da shi, sai yă tuɓe lulluɓin har sai ya fito.
Kuma duk sa’ad da ya fito yă faɗa wa Isra’ilawa abin da aka umarce shi, 35 sai su ga
fuskarsa tana ƙyalli. Sa’an nan Musa yă sāke lulluɓe fuskarsa, har sai ya shiga don
yă yi magana da UBANGIJI.

## 35

### *Ka’idodin Asabbaci*

1 Musa ya tara dukan jama’ar Isra’ilawa ya ce musu, “Waɗannan su ne abubuwan
da UBANGIJI ya umarce ku, ku yi. 2 Kwana shida za ku yi aiki, amma rana ta bakwai
za tă zama rana mai tsarki, Asabbaci ne na hutu ga UBANGIJI. Duk wanda ya yi aiki a
wannan rana dole a kashe shi. 3 Kada ku hura wuta a cikin duk mazauninku a ranar
Asabbaci.”

### *Kayayyaki don tabanakul*
*(Fitowa 25.1-9; 35.10-19)*

4 Musa ya ce wa dukan jama’ar Isra’ilawa, “Ga abin da UBANGIJI ya umarta. 5 Daga
cikin abin da kuke da shi, ku ɗauki kyauta domin UBANGIJI, duk wanda yana niyya,
sai yă kawo wa UBANGIJI kyauta ta,

“zinariya, azurfa da tagulla;

[6] shuɗi, shunayya da jan zare, lallausan lilin,
da gashin akuya;
[7] fatun rago da aka rina ja, da fatun shanun teku; da itacen ƙirya
[8] da man zaitun don fitila; da kayan yaji don man shafewa, da kuma turare mai ƙanshi;
[9] duwatsun onis, da sauran duwatsu masu daraja waɗanda za a mammanne a efod da ƙyallen maƙalawa a ƙirji.

[10] "Duk waɗanda suke da fasaha a cikinku, su zo su yi dukan abin da UBANGIJI ya umarta,

[11] "wato, aikin tabanakul da tentinsa tare da murfinsa, maɗauransa, katakansa, sandunansa da tussansa;
[12] akwatin alkawari da sandunansa, murfin kafara da labulen da ya rufe shi;
[13] tebur da sandunansa, da dukan kayansa da kuma burodin kasancewa;
[14] wurin ajiye fitila da yake don fitilu da kayayyakinsa, fitilu da mai don fitila;
[15] bagaden turare da sandunansa, man shafewa da turare mai ƙanshi; da labulen ƙofar shiga tabanakul;
[16] bagaden hadaya ta ƙonawa da rigarsa ta tagulla da sandunansa da duk kayayyakinsa, daron tagulla da wurin ajiye shi.
[17] Labulen filin tenti da sandunansa da tussansa, da kuma labulen ƙofar shiga fili;
[18] turakun tenti don tabanakul da kuma don filin, da igiyoyinsu;
[19] saƙaƙƙun riguna na sawa don hidima cikin wuri mai tsarki da tsarkakakkun riguna na Haruna firist, da riguna don 'ya'yansa maza lokacin da suke aiki a matsayin firistoci."

[20] Sai dukan jama'ar Isra'ilawa suka janye daga fuskar Musa, [21] duk waɗanda suke
da niyya, waɗanda kuma zukatansu suka motsa su, suka kawo kyautai wa UBANGIJI,
don aikin Tentin Sujada, don duk aikinsa, da don tsarkakakkun riguna. [22] Duk
waɗanda suke da niyya, maza da mata, gaba ɗaya, suka kawo kayan ado na zinariya
na kowane iri. 'Yan kunne, da ƙawane, da mundaye, da kayayyakin zinariya iri-iri.
Dukansu suka miƙa zinariyarsu a matsayin hadaya ga UBANGIJI. [23] Kowane mutumin
da yake da shuɗi, shunayya ko jan zare, ko lallausan lilin, ko gashin akuya, ko fatun
rago da aka rina ja, ko fatun shanun teku, suka kawo. [24] Masu miƙa kyautar azurfa,
ko tagulla suka kawo su a matsayin kyautai ga UBANGIJI, kuma kowane mutumin da
yake da itacen ƙirya don kowane sashin aikin, ya kawo. [25] Kowace mace mai fasaha
ta kaɗa zare da hannuwanta, ta kuma kawo abin da ta kaɗa na shuɗi, shunayya,
ko jan zare, ko lallausan lilin. [26] Kuma dukan matan da suke da niyya, suke kuma
da fasaha, suka kaɗa gashin akuya. [27] Shugabannin suka kawo duwatsun Onis. Da
duwatsu masu daraja don a jera a kan efod da ƙyallen maƙalawa a ƙirji. [28] Suka
kawo kayan yaji da man zaitun don fitila da don man shafewa da kuma don turare
mai ƙanshi. [29] Dukan mazan Isra'ilawa da matan da suke da niyya suka kawo wa
UBANGIJI kyautai na yardar rai, domin dukan aikin da UBANGIJI ya umarce su ta bakin
Musa.

*Bezalel da Oholiyab*
*(Fitowa 31.1-11)*

[30] Sa'an nan ya ce wa Isra'ilawa, "Duba UBANGIJI ya zaɓi Bezalel ɗan Uri, ɗan Hur,
daga kabilar Yahuda, [31] ya kuma cika shi da Ruhun Allah, da fasaha, azanci da kuma
sani cikin dukan sana'ar hannu, [32] don yă ƙirƙiro zāne-zāne na gwaninta waɗanda
za yi da zinariya, da azurfa da kuma tagulla. [33] Haka kuma wajen sassaƙar duwatsu

na jerawa, da sassaƙar itace, da kowane irin aiki na gwaninta. 34 Ya kuma ba Bezalel
da Oholiyab ɗan Ahisamak, daga kabilar Dan, iyawa don koya wa waɗansu. 35 Ya
cika su da fasaha don yin kowane irin aikin sana'a, zāne-zāne, ɗinke-ɗinke shuɗi,
shunayya da jan zare, da lallausan lilin, da kuma masu yin saƙa, sun gwaninta ƙwarai
cikin kowane irin aikin hannu da kuma zāne-zāne.

# 36

1 Saboda haka Bezalel, Oholiyab da kowane mutumin da UBANGIJI ya ba shi basira
da iyawa, na sanin yadda za a yi duk aikin shirya wuri mai tsarki, za su yi aiki yadda
UBANGIJI ya umarta."
2 Sa'an nan Musa ya kira Bezalel da Oholiyab da kowane mutumin da UBANGIJI
ya ba shi iyawa da kuma wanda ya yi niyya yă yi aiki. 3 Suka karɓa daga wurin
Musa dukan kyautai da Isra'ilawa suka kawo don su yi aikin shirya wuri mai tsarki.
Mutane suka ci gaba da kawo kyautai yardar rai kowace safiya. 4 Sai dukan masu
fasaha waɗanda suke aikin wuri mai tsarki suka ɗan dakata 5 suka ce wa Musa,
"Mutane suna kawo fiye da abin da ake bukata domin aikin da UBANGIJI ya umarta
a yi."
6 Sai Musa ya ba da umarni, suka aika ko'ina a cikin sansani cewa, "Kada namiji
ko ta mace yă sāke kawo kyauta don wuri mai tsarki." Ta haka mutane suka daina
kawowa. 7 Saboda abin da suke da shi ya fi abin da ake bukata domin aikin.

### *Tabanakul*
### *(Fitowa 26.1-14)*

8 Dukan maza masu fasaha a cikin sauran masu aikin suka yi tabanakul da labule
goma na tuƙaƙƙun lallausan lilin na shuɗi, da shunayya, da jan zare, aka yi wa
labulen zānen kerubobi na gwaninta. 9 Tsawon kowane labule, kamu ashirin da
takwas ne, fāɗinsa kuma kamu huɗu. Dukan labulen, girmansu ɗaya ne. 10 Suka
ɗinɗinke labule biyar a harhaɗe, suka kuma yi haka da sauran labule biyar ɗin.
11 Suka yi rami a gefe-gefen labulen da zaren ruwan bula, haka kuma suka yi da
ɗayan gefen na biyu ɗin. 12 Suka kakkafa rammuka hamsin a daidai bakin labulen,
haka kuma suka yi a kan labule na biyun. Haka aka ɗaɗɗaura rammukan nan da
junansu yă zama kamar abu guda. 13 Sa'an nan suka yi maɗaurai hamsin na zinariya,
suka yi amfani da su don daurin kashi biyu na labulen saboda tabanakul yă zama
ɗaya.
14 Suka yi labule da gashi akuya goma sha ɗaya don tenti a bisa tabanakul. 15 Dukan
labule goma sha ɗayan girmansu ɗaya ne, tsawonsa kamu talatin, fāɗinsa kuma
kamu huɗu ne. 16 Suka harhaɗa labule biyar wuri ɗaya, suka kuma harhaɗa shida
wuri ɗaya. 17 Sa'an nan suka yi rammuka hamsin a gefen labule na kashe na farko,
haka kuma a gefen labule na ƙarshen na kashi biyar. 18 Suka yi maɗaurin tagulla
hamsin don su ɗaura tenti yă zama ɗaya. 19 Sai suka yi wa tentin murfi da fatun rago
da aka rina ja, a bisa wannan kuwa akwai murfin fatun shanun teku.

### *(Fitowa 26.15-30)*

20 Suka yi katakan tabanakul da itacen ƙirya. 21 Tsawon kowane katako kamu
goma ne, kaurinsa kuma kamu ɗaya da rabi, 22 tare da katakai a fiƙe ɗaura da juna.
Haka suka yi da dukan katakan tabanakul. 23 Suka yi katakai ashirin don gefen
kudu na tabanakul 24 suka kuma yi rammukan azurfa arba'in don katakan su shiga
ƙarƙashinsu, rammuka biyu domin kowane katako, ɗaya ƙarƙashin kowanne da
aka fiƙe. 25 A ɗaya gefen, gefen arewa na tabanakul, suka yi katakai ashirin 26 da
rammuka arba'in na azurfa, biyu-biyu don kowane katako. 27 Suka yi katako shida
don iyaka ta ƙarshe, wato, gefen yamma na tabanakul, 28 aka kuma yi katakai biyu
domin kusurwoyi tabanakul a iyaka ta ƙarshe. 29 A waɗannan kusurwoyi biyu, an

ninka katakan sau biyu daga ƙasa har sama, aka kuma sa su cikin zobe guda; dukansu
biyu an yi su daidai. 30 Ta haka aka sami katakai takwas da rammukan azurfa goma
sha shida, biyu-biyu a ƙarƙashin kowane katako.
31 Suka kuma yi sanduna na itace ƙirya, biyar domin katakan da suke a gefe guda na
tabanakul, 32 biyar domin waɗanda suke ɗayan gefen da kuma biyar domin katakan
da suke gefen yamma na iyaka ta ƙarshen tabanakul. 33 Suka sa sandan da yake
a tsakiya yă wuce daga wannan gefe zuwa wancan. 34 Sai suka dalaye katakan da
zinariya, suka yi zoban zinariya don su riƙe sandunan. Suka kuma dalaye sandunan
da zinariya.

*(Fitowa 26.31-37)*

35 Suka kuma yi labule da shuɗi, shunayya, jan zare, da kuma lallausan lilin, suka
kuma yi wa labulen zānen kerubobi na gwaninta. 36 Suka yi dogayen sanduna huɗu
na itacen ƙirya dominsa, suka dalaye su da zinariya. Suka yi ƙugiya na zinariya
dominsa, suka yi rammuka huɗu da azurfa. 37 Suka yi wa ƙofar tenti labulen shuɗi,
shunayya, jan zare, da kuma lallausan lilin, aikin gwaninta; 38 suka kuma yi dogayen
sanduna biyar da ƙugiya dominsu. Suka dalaye saman dogayen sandunan da abin
daurinsu da zinariya, suka kuma yi rammukansu guda biyar da tagulla.

# 37

*Akwatin alkawari*
*(Fitowa 25.10-22)*

1 Bezalel ya yi akwatin alkawari da itacen ƙirya, tsawonsa kamu biyu da rabi,
fāɗinsa kamu ɗaya da rabi, tsayinsa kamu ɗaya da rabi. 2 Ya dalaye shi da zinariya
zalla, ciki da waje, ya kuma yi zubin zinariya kewaye da shi. 3 Ya yi masa zubi huɗu
na zoban zinariya, ya kuma ɗaura su a ƙafafunsa huɗu, zobai biyu a wannan gefe
da kuma biyu a wancan. 4 Sa'an nan ya yi sanduna na itacen ƙirya, ya dalaye shi
da zinariya. 5 Sai ya sa sandunan a cikin rammukan da suke gefen Akwatin don
ɗaukarsa.
6 Ya yi murfin jinƙai da zinariya zalla, wato, tsawonsa ƙafa biyu, fāɗinsa kuma
ƙafa ɗaya da rabi. 7 Sa'an nan ya yi kerubobi biyu da ƙeraren zinariya a ƙarshen
murfin jinƙan. 8 Ya yi kerub a iyakar gefe ɗaya, ya yi ɗayan kuma a wancan gefe;
a iyakan nan biyu, ya yi su a haɗe da murfin. 9 Kerubobin suka buɗe fikafikansu
sama, suka inuwatar da murfin da fikafikansu. Kerubobin suna fuskantar juna, suna
kuma kallon murfin.

*Tebur*
*(Fitowa 25.23-30)*

10 Suka yi tebur da itacen ƙirya, tsawonsa ƙafa biyu, fāɗinsa ƙafa ɗaya, tsayinsa
kuma ƙafa ɗaya da rabi. 11 Sa'an nan suka dalaye shi da zinariya zalla, suka kuma yi
zubi na zinariya kewaye da shi. 12 Suka kuma yi masa baki mai fāɗin tafi hannu, suka
yi zubin zinariya a bisa bakin. 13 Suka yi zubin zobai huɗu na zinariya don tebur
ɗin, sai suka ɗaura su a kusurwoyi huɗu inda ƙafafu huɗun suke. 14 Sa'an nan aka
sa zoban kurkusa da bakin don riƙe sandunan da ake amfani da su wurin ɗaukan
teburin. 15 An yi sandunan da ake ɗaukan tebur da itacen ƙirya, aka kuma dalaye su
da zinariya. 16 Suka kuma yi duk kayayyakin teburin da zinariya zalla, farantansa,
kwanonin tuya, kwanoninsa, da kuma butoci domin hadaya ta sha.

*Wurin ajiye fitila*
*(Fitowa 25.31-40)*

17 Suka yi wurin ajiye fitila da zinariya zalla, suka yi gindinsa da kuma gorar jikinsa,
da ƙerarriyar zinariya. Kwaf wurin ajiye fitila da mahaɗansa, da furanninsa, a haɗe
aka yi su da wurin ajiye fitilan. 18 Akwai rassa guda shida da suka miƙe daga gefe

wurin ajiyar fitilar, uku a wannan gefe, uku kuma a wancan. [19] A reshe guda na wurin
ajiye fitilan, akwai kwaf uku masu kama da tohon almon, akwai kuma uku a reshe
na biye, haka kuma suke a dukan rassa shida da suke daga wurin ajiye fitilan. [20] A
bisa wurin ajiye fitilan kuma akwai kwaf huɗu da aka yi su kamar furannin almon
da toho da kuma mahaɗai. [21] Toho ɗaya yana a ƙarƙashin rassa biyu waɗanda suke
daga wurin ajiye fitilan, toho na biyu yana a ƙarƙashin rassa biyu na biye, toho na
uku kuma yana a ƙarƙashin rassa biyu na uku, duka-duka rassa shida ne. [22] An ƙera
mahaɗai da rassa wurin ajiye fitila a haɗe. Da ƙerarriyar zinariya aka yi wurin ajiye
fitilar da dukan komensa a haɗe.
[23] Da zinariya zalla suka yi fitilu bakwai, da hantsuka da farantansa. [24] Daga talenti
ɗaya na zinariya zalla suka yi wurin ajiye fitila da dukan kayayyakinsa.

*Bagaden ƙona turare*
*(Fitowa 30.1-5)*
[25] Suka yi bagaden ƙona turare da itacen ƙirya. Shi bagaden, murabba'i ne,
tsawonsa kamu ɗaya, fāɗinsa kamu ɗaya, tsayinsa kuma kamu biyu, ƙahoninsa kuwa
a haɗe suke da shi. [26] Suka dalaye saman da dukan gefe-gefen da kuma ƙahonin da
zinariya zalla, suka kuma yi zubin zinariya kewaye da shi. [27] Suka yi zobai biyu na
zinariya a ƙarƙashin zubin, biyu-biyu ɗaura da juna, don su riƙe sandunan da za a
ɗauka shi. [28] Suka yi sandunan da itacen ƙirya, suka kuma dalaye su da zinariya.
*(Fitowa 30.22-38)*
[29] Suka kuma yi tsattsarkan mai na shafewa da kuma zalla turare mai ƙanshi,
yadda mai yin turare yakan yi.

# 38

*Bagaden hadaya ta ƙonawa*
*(Fitowa 27.1-8)*
[1] Suka gina bagaden ƙona hadaya da itacen ƙirya, tsawonsa kamu biyar, fāɗinsa
kamu biyar, murabba'i ke nan, tsayinsa kuwa kamu uku. [2] Suka yi ƙahoni a
kusurwansa huɗu, ƙahonin da bagade a haɗe suke, suka kuma dalaye bagaden da
tagulla. [3] Da tagulla kuma ya yi duk kayayyakin bagaden, da kwanoni, da babban
cokali, da daruna, da cokula masu yatsotsi, da farantan wuta. [4] Suka yi wa bagaden
raga, tagulla kuma don yǎ sa shi a tsakiya. [5] Suka yi zubin zoban tagulla don riƙe
sanduna a kusurwoyi huɗu na ragar tagullar. [6] Suka yi sanduna da itacen ƙirya, suka
kuma dalaye su da tagulla. [7] Suka sa sandunan a cikin zoban saboda su kasance a
gefen bagade don ɗaukarsa, suka yi rami cikinsa.

*Kwano don wanki*
*(Fitowa 30.18-21)*
[8] Suka yi daro da gammonsa da tagulla daga madubai na mata masu yin aiki a
ƙofar Tentin Sujada.

*Filin tabanakul*
*(Fitowa 27.9-19)*
[9] Suka kuma yi filin Tentin Sujada. Suka yi labulanta na gefen kudu da lallausan
lilin, tsawonsu kamu ɗari, [10] da sanduna ashirin da rammukan sandunan tagulla
ashirin, da kuma ƙugiyoyin azurfa da maɗauri a kan sandunan. [11] Tsawon labule na
wajen gefen arewa kamu ɗari ne, yana kuma da sanduna guda ashirin da rammuka
ashirin na tagulla, da ƙugiyoyin azurfa da maɗaurai a kan sandunan.
[12] Labule na gefen yamma kamu hamsin, da sanduna guda goma, da rammuka
guda goma, da ƙugiyoyin azurfa da maɗaurai a kan sandunan. [13] A ƙarshen gefen
gabas, wajen fitowar rana, shi ma fāɗinsa kamu hamsin ne. [14] Labule na gefe ɗaya

na ƙofar, kamu goma sha biyar ne, da sanduna guda uku da rammukansu, 15 akwai
labule mai kamu goma sha biyar a ɗayan gefen ƙofar shiga zuwa filin Tentin Sujada,
da sanduna uku da rammuka uku. 16 An yi dukan labulan da suke kewaye da filin
Tentin Sujada da lallausan zaren lilin. 17 An yi rammukan sandunan da tagulla. An
dalaye ƙugiyoyi da maɗauran da suke kan sandunan da azurfa; saboda haka dukan
sandunan filin Tentin Sujada suna da maɗaurai na azurfa.
18 Aka yi wa labulen ƙofar filin Tentin Sujada ado na ɗinki da na shuɗi, da na
shunayya, da na jan zare, da na lallausan lilin, aikin gwaninta. Tsawonsa kamu
ashirin, kuma kamar yadda labulen filin Tentin Sujada suke, tsayinsa kamu biyar
ne, 19 da sanduna guda huɗu da rammuka guda huɗu na tagulla. Kugiyoyinsu da
maɗauransu na azurfa ne, aka kuma dalaye bisansu da azurfa. 20 Aka yi dukan
ƙarafan kafa tabanakul da kuma na kewayen filin Tentin Sujada da tagulla ne.

### *Kayayyakin da aka yi amfani da su*

21 Waɗannan su ne kayayyakin da aka yi amfani da su domin aikin tabanakul, da
tabanakul na Shaida, waɗanda aka rubuta bisa ga umarnin Musa ta wurin Lawiyawa,
a ƙarƙashin jagorancin Itamar ɗan Haruna, firist. 22 (Bezalel ɗan Uri, ɗan Hur, na
kabilar Yahuda, ya yi dukan abin da UBANGIJI ya umarci Musa; 23 tare da shi akwai
Oholiyab ɗan Ahisamak, na kabilar Dan, shi gwani ne cikin aikin zāne-zāne, da ɗinki
na shuɗi, da na shunayya, da na jan zare, da na lallausan lilin.) 24 Jimillar zinariya
daga hadaya ta kaɗawar da aka yi amfani da su domin aikin wuri mai tsarki ta kai
talenti 29 da shekel 730, bisa ga ma'aunin shekel na tsattsarkan wuri.
25 Azurfar da aka samu daga ƙidayar taron jama'a, talenti 100 ne, da shekel 1,775,
bisa ga ma'aunin shekel na tsattsarkan wuri. 26 Duk mutumin da ya shiga ƙirge daga
mai shekaru ashirin zuwa gaba, ya ba da rabin shekel. Mazan da suka shiga ƙirge
sun kai mutum 603,550. 27 An yi amfani da azurfa talenti 100 don yin rammuka na
wuri mai tsarki, da kuma rammukan labule, rammuka 100 daga talenti 100, talenti
ɗaya don rami ɗaya. 28 Suka yi amfani da shekel 1,775 don yin ƙugiyoyi saboda
sanduna, suka dalaye bisan sandunan da maɗauransu.
29 Tagullar da aka bayar daga hadaya ta kaɗawa ya kai talenti 70 da shekel 2,400.
30 Suka yi amfani da shi don yin rammukan ƙofar Tentin Sujada, da bagaden tagulla
tare da ragar tagulla da dukan kayayyakinsa, 31 da rammukan sanduna don kewaye
filin, da waɗanda suke ƙofarsa, da dukan ƙarafan kafa tenti don tabanakul, da kuma
don kewaye filin.

# 39

### *Rigunan firistoci*
### *(Fitowa 28.1-14)*

1 Daga zare mai ruwan shuɗi, da shuɗayya da kuma jan zare suka yi tsarkaken
rigunan domin hidima a wuri mai tsarki. Suka kuma yi tsarkaken riguna don Haruna,
yadda UBANGIJI ya umarci Musa.

### *Efod*

2 Suka yi efod na zinariya, da shuɗi, da shunayya, da jan zare, da kuma lallausan
lilin. 3 Suka bubbuga zinariya ta zama falle, suka yayyanka ta zare-zare don su yi
saƙa da ita, tare da zane na shuɗi, da na shunayya, da na jan zare, da na lallausan
lilin, aikin gwani mai fasaha. 4 Suka yi wa efod kafaɗu, sa'an nan suka haɗa su a
gefenta biyu na sama, don a iya ɗaurawa. 5 Gwanin mai saƙa ya saƙa abin ɗamarar
efod. Da irin kayan da aka saƙa efod ne aka saƙa abin ɗamarar, wato, da zinariya, da
shuɗi, da shunayya, da jan zare, da zaren lallausan lilin, yadda UBANGIJI ya umarci
Musa.

6 Suka shimfiɗa duwatsun onis, suka jera su cikin tsaiko na zinariya, suka kuma
zāna sunayen ’ya’yan Isra’ila a kan duwatsun kamar yadda akan yi hatimi. 7 Sa’an
nan suka ɗaura su a ƙyallen kafaɗun efod a matsayin duwatsun tuni wa ’ya’yan
Isra’ila, yadda UBANGIJI ya umarci Musa.

### *Kyallen maƙalawa a ƙirji*
### *(Fitowa 28.15-30)*

8 Suka yi ƙyallen maƙalawa a ƙirji, aikin gwani. Suka yi shi kamar efod, na
zinariya, da na shuɗi, da na shunayya, da na jan zare, da kuma na lallausan lilin.
9 Kyallen maƙalawa a ƙirjin murabba’i ne, aka ninka shi biyu, tsawonsa da fāɗinsa
kamu ɗaya-ɗaya ne. 10 Sa’an nan suka sa jeri huɗu na duwatsu masu daraja a
bisansa. A jeri na farko akwai yakutu, da tofaz, da zumurrudu; 11 a jeri na biyu
akwai turkuwoyis, da saffaya, da daimon; 12 a jeri na uku akwai yakinta, da idon
mage, da ametis; 13 a jeri na huɗu akwai beril, da onis, da yasfa. Aka sa su cikin
tsaiko na zinariya. 14 Aka zāna duwatsu goma sha biyu, ɗaya don kowane sunan
’ya’yan Isra’ila goma sha biyu, kamar yadda akan yi hatimi.
15 Sai suka yi tuƙaƙƙun sarƙoƙi na zinariya zalla a kan ƙyallen maƙalawa a ƙirji.
16 Suka yi tsaiko biyu na zinariya da zoban zinariya biyu, suka kuma ɗaura zoban a
kusurwoyi biyu na ƙyallen maƙalawa a ƙirji. 17 Suka ɗaura sarƙoƙi biyu na zinariya
da kusurwoyi na ƙyallen maƙalawa a ƙirji. 18 Suka maƙala waɗancan bakin sarƙoƙin
zinariya a tsaikon nan biyu, sa’an nan suka rataya su a kafaɗun efod daga gaba.
19 Suka yi zobai biyu na zinariya suka haɗa, suka sa su a gefe biyu na ƙyallen
maƙalawa a ƙirji daga ciki kusa da efod. 20 Sa’an nan suka yi waɗansu ƙarin zobai
biyu na zinariya, suka maƙale su daga ƙasa a gaban kafaɗu biyu na efod kusa da
mahaɗin a bisa abin ɗamarar efod. 21 Suka ɗaura zoban ƙyallen maƙalawa a ƙirjin a
zoban efod da shuɗiyar igiya don ƙyallen maƙalawa a ƙirji, ya kwanta lif a bisa kan
abin ɗamarar efod don kada yǎ kunce daga efod, sun yi yadda UBANGIJI ya umarci
Musa.

### *Sauran rigunan firistoci*
### *(Fitowa 28.31-43)*

22 Suka kuma saƙa taguwa ta efod da shuɗi duka, aikin gwani mai saƙa, 23 an yi
wa taguwar wuyan wundi a tsakiya kamar sulke, aka daje wuyan don kada yǎ kece.
24 Suka yi fasalin ’ya’yan rumman da shuɗi, da shunayya, da jan zare, da lallausan
lilin kewaye da gefe-gefen taguwar. 25 Suka yi ƙararrawa da zinariya zalla, suka
sa su a tsakanin fasalin ’ya’yan rumman kewaye da gefe-gefen taguwa. 26 Aka jera
ƙararrawan da ’ya’yan rumman bi da bi. Haka aka jera su kewaye da gefe-gefen
taguwar aiki, yadda UBANGIJI ya umarci Musa.
27 Suka saƙa doguwar riga da lallausan lilin don Haruna da ’ya’yansa, aikin gwani
mai saƙa, 28 suka yi rawanin da lallausan lilin, da hulan lilin da rigunan ciki na
lallausan lilin. 29 Suka yi abin ɗamara da lallausan lilin da shuɗi, shunayya da jan
zare, aikin gwanin mai ɗinki, yadda UBANGIJI ya umarci Musa.
30 Suka yi allo tsattsarka da zinariya tsantsa, suka zāna rubutu irin na hatimi a
kansa haka,

Mai tsarki ga UBANGIJI.

31 Sa’an nan suka ɗaura shi da shuɗiyar igiya a gaban rawanin, yadda UBANGIJI ya
umarci Musa.

### *Musa ya duba tabanakul*
### *(Fitowa 35.10-19)*

32 Ta haka aka gama dukan aikin tabanakul da Tentin Sujada. Isra’ilawa suka yi
kome yadda UBANGIJI ya umarci Musa.

33 Sa’an nan suka kawo wa Musa tabanakul, tentin da dukan kayayyakinsa,
ƙugiyoyinsa, katakansa, da sandunansa, da dogayen sandunansa da ram-
mukansa;
34 murfi na fatun rago wanda aka rina ja, da murfi na fatun shanun teku; da kuma
laɓulen
35 akwatin Alkawari da sandunansa da murfin kafara;
36 tebur da dukan kayayyakinsa, da burodin Kasancewa;
37 wurin ajiye fitilu na zinariya zalla, da jerin fitilunsa da dukan kayayyakinsa, da
man fitila,
38 bagade na zinariya, da man shafewa, da turare mai ƙanshi, da labulen ƙofar
shiga tenti,
39 bagade na tagulla na raga, da sandunansa da kayan aikinsa; da daro da wurin
ajiyarsa,
40 labulen filin, sandunansa da rammukansa, labulen ƙofar shiga filin; igiyoyi da
ƙarafan kafa filin; dukan kayan aikin tabanakul da Tentin Sujada;
41 da kuma saƙaƙƙun rigunan da ake sawa don hidima a wuri mai tsarki, duk
da tsarkakan riguna na Haruna firist da rigunan ’ya’yansa maza, sa’ad da suke
hidima a matsayin firistoci.

42 Isra’ilawa suka yi dukan aikin nan yadda UBANGIJI ya umarci Musa. 43 Musa ya
duba aikin, sai ya ga cewa sun yi shi daidai yadda UBANGIJI ya umarta. Sai Musa ya
sa musu albarka.

# 40

### *Kafawa tabanakul*

1 Sa’an nan UBANGIJI ya ce wa Musa, 2 “Ka kafa tabanakul, da Tentin Sujada, a kan
rana ta fari ga watan fari. 3 Ka sa akwatin Alkawari a cikinsa, sa’an nan ka rufe shi
da labule. 4 Ka shigar da teburin ka shirya kayayyakin a kansa. Sa’an nan ka shigar
da wurin ajiye fitilan ka kuma sa fitilunsa. 5 Ka sa bagaden zinariya na ƙona turare
a gaban akwatin Alkawari, ka kuma sa labule a ƙofar shiga tabanakul.

6 “Ka ajiye bagade na yin hadaya ta ƙonawa a gaban ƙofar tabanakul, da Tentin
Sujada; 7 ka ajiye daron tsakanin Tentin Sujada da bagaden, ka kuma zuba ruwa a
cikinsa. 8 Ka yi fili kewaye da shi, ka kuma sa labule a ƙofar shiga filin.

9 “Ka ɗauki man shafewa ka shafe tabanakul da duka abin da yake cikinsa; ka keɓe
shi da dukan kayayyakinsa, zai zama tsarkake. 10 Sa’an nan ka shafe bagaden hadaya
ta ƙonawa da kayansa; ka keɓe bagaden, zai zama mai tsarki. 11 Ka shafe daron da
wurin ajiyarsa, ka kuma keɓe su.

12 “Ka kawo Haruna da ’ya’yansa a ƙofar Tentin Sujada ka wanke su da ruwa.
13 Sa’an nan ka sa wa Haruna tsarkakun riguna, ka shafe shi, ka kuma keɓe shi don
yă yi mini hidima a matsayin firist. 14 Ka kawo ’ya’yansa maza ka sa musu taguwoyi.
15 Ka shafe su yadda ka shafe mahaifinsu, don su yi mini hidima a matsayin firistoci.
Shafe musu man, zai sa su zama firistoci na ɗinɗinɗin, dukan zamanansu.” 16 Musa
ya aikata dukan kome yadda UBANGIJI ya umarce shi.

17 Da haka aka kafa tabanakul, a rana ta fari ga wata na fari a shekara ta biyu.
18 Sa’ad da Musa ya kafa tabanakul, ya sa rammuka a wurinsu, ya sa katakan, ya
kuma sa sandunan, ya kakkafa dogayen sandunan. 19 Sa’an nan ya shimfiɗa tentin
a bisa tabanakul, ya kuma sa murfi a bisa tentin, yadda UBANGIJI ya umarce shi.

20 Ya ɗauki dokokin Alkawari ya sa a cikin akwatin, ya kuma zura sandunan a
zoban akwatin, sa’an nan ya sa murfin kafara a bisansa. 21 Sai ya kawo akwatin a

cikin tabanakul, ya kuma rataye labulen rufewa ya tsare akwatin Alkawarin, yadda
UBANGIJI ya umarce shi.
22 Musa ya sa teburin a Tentin Sujada, a gefen arewa na tabanakul waje da labulen.
23 Ya shirya burodin a kai a gaban UBANGIJI, yadda UBANGIJI ya umarce shi.
24 Ya sa wurin ajiye fitilan a Tentin Sujada ɗaura da teburin a gefen kudu na
tabanakul 25 ya kuma shirya fitilun a gaban UBANGIJI, yadda UBANGIJI ya umarce shi.
26 Musa ya sa bagaden zinariya a cikin Tentin Sujada a gaban labulen 27 ya ƙone
turare mai ƙanshi a kai, yadda UBANGIJI ya umarce shi.
28 Sa'an nan ya sa labule a ƙofar shiga na tabanakul. 29 Ya sa bagaden hadaya
ta ƙonawa kusa da ƙofar tabanakul, Tentin Sujada, sa'an nan ya miƙa hadaya ta
ƙonawa da hadaya ta gari a kansa, yadda UBANGIJI ya umarce shi.
30 Ya sa daro tsakanin Tentin Sujada da bagade, ya kuma zuba ruwa a cikinsa don
wanki, 31 a cikin kuwa Musa da Haruna da 'ya'yansa maza sukan wanke hannunsa
da ƙafafunsu. 32 Sukan yi wanka a duk sa'ad da suka shiga Tentin Sujada, ko in suka
kusaci bagade, yadda UBANGIJI ya umarci Musa.
33 Sa'an nan Musa ya yi fili kewaye da tabanakul da kuma bagaden, ya rataye labule
a ƙofar shiga filin. Da haka Musa ya gama aikin.

### *Ɗaukakar UBANGIJI*

34 Sa'an nan girgije ya rufe Tentin Sujada sai ɗaukakar UBANGIJI ta cika tabanakul.
35 Musa bai iya shiga Tentin Sujada ba domin girgije ya riga ya sauka a kansa,
ɗaukakar UBANGIJI kuwa ta cika tabanakul.
36 Cikin tafiyar Isra'ilawa duka, sukan kama tafiyarsu ne a duk sa'ad da girgijen ya
tashi daga kan tabanakul. 37 Idan girgijen bai tashi ba, ba za su tashi ba, sai a ranar
da ya tashi. 38 Gama a cikin tafiyarsu duka, girgijen Ubangiji yana kan tabanakul da
rana, da dare kuwa wuta yake cikinsa domin dukan Isra'ilawa su gani.

# Firistoci

*Hadaya ta ƙonawa*

1 UBANGIJI ya kira Musa ya yi masa magana daga cikin Tentin Sujada ya ce,
2 "Yi magana da Isra'ilawa ka ce musu, 'Duk sa'ad da waninku ya kawo hadaya
ga UBANGIJI, ku kawo hadayarku ta dabba daga garkenku ta shanu ko kuwa daga
tumakinku.
3 " 'In hadaya ta ƙonawar daga shanu ne, sai yă miƙa namiji marar lahani. Dole
yă kawo shi a ƙofar Tentin Sujada don yă zama yardajje ga UBANGIJI. 4 Zai ɗibiya
hannunsa a kan hadaya ta ƙonawar, za a kuwa karɓa a madadinsa don a yi kafara
dominsa. 5 Zai yanka ɗan bijimin a gaban UBANGIJI, Haruna kuwa da 'ya'yansa maza
firist, za su kawo jinin su kuma yafa shi a kan bagaden a kowane gefe a mashigin
Tentin Sujada. 6 Zai feɗe hadaya ta ƙonawar, yă yayyanka shi gunduwa-gunduwa.
7 'Ya'yan Haruna maza waɗanda suke firistoci za su hura wuta a bagade, su kuma
shirya itace a kan wutar. 8 Sa'an nan 'ya'yan Haruna maza waɗanda suke firistoci za
su shirya gunduwa-gunduwar haɗe da kan da kuma kitsen a kan itace mai cin wuta
wanda yake a kan bagaden. 9 Zai wanke kayan cikin da kuma ƙafafun da ruwa, firist
ɗin kuwa zai ƙone dukan waɗannan a kan bagade. Hadaya ce ta ƙonawa, hadaya
ce kuma wadda aka yi da wuta, mai daɗin ƙanshi ga UBANGIJI.
10 " 'In hadaya ta ƙonawar daga garke ne, ko na tumaki, ko na awaki, zai miƙa
namiji ne marar lahani. 11 Zai yanka shi a gefen arewa na bagaden a gaban UBANGIJI,
'ya'yan Haruna firistoci kuwa za su yayyafa jinin dabbar a bagaden a kowane gefe.
12 Zai yanka shi gunduwa-gunduwa, firist kuwa zai shirya su haɗe da kan, da kuma
kitsen a kan itace mai cin wutar da yake a kan bagade. 13 Zai wanke kayan cikin
da kuma ƙafafun da ruwa, firist ɗin kuwa zai ƙone dukan waɗannan a kan bagade.
Hadaya ce ta ƙonawa, hadaya ce kuma wadda aka yi da wuta, mai daɗin ƙanshi ga
UBANGIJI.
14 " 'In hadaya ga UBANGIJI ɗin, hadaya ta ƙonawa ta tsuntsaye ce, zai miƙa kurciya
ko 'yar tattabara. 15 Firist zai kawo ta bagade, yă murɗe wuyan tsuntsun yă ƙone shi
a kan bagade; zai tsiyaye jininsa tsuntsun a gefen bagaden. 16 Amma zai ɗauki kayan
cikin tsuntsun da gashin yă zubar da su a gefen bagaden a wajen gabas a wurin zuba
toka. 17 Zai tsaga shi biyu a tsaka, amma ba zai raba shi ba. Firist ɗin zai ɗibiya shi
a bisa itacen da yake bisa bagaden, yă ƙone shi. Hadaya ce ta ƙonawa, hadaya ce
kuma wadda aka yi da wuta, mai daɗin ƙanshi ga UBANGIJI.

## 2

*Hadaya ta hatsi*

1 " 'Sa'ad da wani ya kawo hadaya ta gari ga UBANGIJI, hadayarsa za tă zama gari
mai laushi ne. Zai zuba mai a kai, yă sa turare a kansa 2 yă kai wa 'ya'yan Haruna
maza waɗanda suke firistoci. Firist zai ɗiba gari mai laushin a tafin hannu da kuma
man, tare da dukan turaren, yă ƙone wannan a sashen tunawa a kan bagade, hadaya
ce da aka yi da wuta, mai daɗin ƙanshi ga UBANGIJI. 3 Sauran hadaya ta garin zai
zama na Haruna da 'ya'yansa; sashe mafi tsarki ne na hadayar da aka yi ga UBANGIJI
ta wuta.
4 " 'In kuka kawo toyayyen hadayar gari da aka yi daga matoya, zai ƙunshi gari mai
laushi, toyayye ba tare da yisti ba, gauraye kuma da mai, ko kuwa ƙosai da aka yi
ba tare da yisti ba, aka kuma kwaɓa da mai. 5 In an toya hadaya ta garinku a kasko,
sai a yi shi da gari mai laushi haɗe da mai, ba kuwa da yisti ba. 6 A gutsuttsura shi,

a zuba mai a kansa, hadaya ce ta hatsi. 7 In hadayarku ta hatsin da aka dafa ne a
tukunya, sai a yi shi da gari mai laushi da kuma mai. 8 A kawo hatsin da aka yi da
waɗannan abubuwa ga UBANGIJI; a ba wa firist wanda zai ɗauka yă kai bagade. 9 Zai
fid da sashen tunawa daga hadaya ta gari, yă ƙone shi a kan bagade kamar hadayar
da ka yi da wuta, mai daɗin ƙanshi ga UBANGIJI. 10 Sauran hadaya ta garin za tă
zama ta Haruna da ’ya’yansa; sashe mafi tsarki ne na hadayun da aka yi ga UBANGIJI
ta wuta.

11 “ ‘Kowace hadaya ta garin da kuka kawo ga UBANGIJI, dole a yi shi ba tare da yisti
ba, gama ba za ku ƙone wani yisti, ko zuma a cikin hadayar da aka yi ga UBANGIJI ta
wuta ba. 12 Za ku iya kawo su ga UBANGIJI kamar hadaya ta ’ya’yan fari, amma ba za
a miƙa su a bagade kamar turare mai ƙanshi ba. 13 A sa gishiri a dukan hadayunku
na hatsi. Kada a rasa sa gishirin alkawari na Allahnku a hadayunku na hatsi, a sa
gishiri a dukan hadayunku.

14 “ ‘In kuka kawo hadaya ta gari na ’ya’yan fari ga UBANGIJI, sai ku miƙa ɓarzajjen
kawunan sabon hatsin da aka gasa a wuta. 15 A sa mai da turare a kansa, hadaya ce
ta hatsi. 16 Firist zai ƙone sashe na ɓarzajjen hatsin da kuma mai, tare da turare don
tunawa, gama hadaya ce da aka ƙone da wuta ga UBANGIJI.

# 3

*Hadaya ta salama*

1 “ ‘In hadayar wani mutum, hadaya ta salama ce,* ya kuma miƙa ’yar dabba daga
garke, ko namiji ko ta mace ce, sai yă miƙa dabbar da ba ta da lahani a gaban UBANGIJI.
2 Yă kuma ɗibiya hannunsa bisa kan hadayarsa, yă yanka ta a mashigin Tentin Sujada.
Sa’an nan ’ya’yan Haruna waɗanda suke firistoci za su yayyafa jinin a kan bagade a
kowane gefe. 3 Daga hadaya ta zumuncin da zai kawo, sai a miƙa waɗannan hadayu
na ƙonawa ga UBANGIJI a wuta; wato, dukan kitsen da ya rufe kayan ciki ko kuwa da
sun shafe su, 4 da ƙodoji biyu tare da kitsen da yake kansu kusa da kwiɓi, da kuma
murfin hanta waɗanda zai cire tare da ƙodoji. 5 ’Ya’yan Haruna za su ƙone shi a kan
bagade a bisa hadaya ta ƙonawa wadda take a kan itacen da yake cin wuta, kamar
hadayar da ka yi da wuta, mai daɗin ƙanshi ga UBANGIJI.

6 “ ‘In ya miƙa dabba ce daga garke a matsayin hadaya ta salama ga UBANGIJI, zai
miƙa namiji ko ta mace marar lahani. 7 In ya miƙa ɗan rago ne, zai kawo shi a gaban
UBANGIJI. 8 Zai ɗibiya hannu a kan hadayarsa, yă yanka shi a gaban Tentin Sujada.
Sa’an nan ’ya’yan Haruna maza za su yayyafa jinin dabbar a kowane gefe na bagade.
9 Daga hadaya ta zumuncin zai kawo, sai a miƙa waɗannan hadayu na ƙonawa ga
UBANGIJI a wuta, wato, kitsen, ƙibabbiya wutsiyar gaba ɗaya da ya yanka gab da
ƙashin gadon baya, dukan kitsen da ya rufe kayan ciki, ko kuwa da suka shafe su,
10 da ƙodoji biyu tare da kitsen da yake kansu kusa da kwiɓi, da kuma murfin hanta
waɗanda zai cire tare da ƙodoji. 11 Firist zai ƙone su a kan bagade kamar hadayar
abinci, wato, hadaya ce da aka ƙone da wuta ga UBANGIJI.

12 “ ‘In yana miƙa akuya ce, zai kawo ta a gaban UBANGIJI. 13 Zai ɗibiya hannunsa
a kanta yă kuma yanka ta a gaban Tentin Sujada. Sa’an nan ’ya’yan Haruna maza
za su yayyafa jininta a kowane gefe na bagade. 14 Daga abin da zai miƙa sai a miƙa
waɗannan hadayu na ƙonawa ga UBANGIJI a wuta, wato, dukan kitsen da ya rufe
kayan cikin, ko kuwa da suka shafe su, 15 da ƙodoji biyu tare da kitsen da yake kansu
kusa da kwiɓi, da kuma murfin hanta waɗanda zai cire tare da ƙodoji. 16 Firist zai
ƙone su a kan bagade kamar abinci, hadaya ce da aka yi da wuta, mai daɗin ƙanshi.
Dukan kitsen na UBANGIJI ne.

* **3:1** Al’adance; hadaya ta zumunci; haka ma a ayoyi 3, 6 da 9.

[17] “ ‘Wannan dawwammamiyar farilla ce ga tsararraki masu zuwa, a inda za ku zauna. Ba za ku ci wani kitse ko wani jini ba.’ ”

# 4

*Hadaya ta zunubi*
*(Firistoci 6.24-30)*

[1] UBANGIJI ya ce wa Musa, [2] “Faɗa wa Isra’ilawa cewa, ‘Sa’ad da wani ya yi zunubi
ba da gangan ba, har ya karya ɗaya daga cikin dokokin UBANGIJI,

[3] “ ‘In shafaffen firist ya yi zunubi, ya jawo wa jama’a laifi, dole yă kawo wa UBANGIJI
ɗan bijimi marar lahani a matsayin hadaya don zunubi saboda zunubin da ya yi.
[4] Zai kawo bijimin a ƙofar Tentin Sujada a gaban UBANGIJI. Zai ɗibiya hannunsa a
kan bijimin, yă kuma yanka shi a gaban UBANGIJI. [5] Sa’an nan shafaffen firist zai ɗiba
jinin bijimin yă kai cikin Tentin Sujada. [6] Yă tsoma yatsarsa a cikin jinin, yă kuma
yafa sau bakwai a gaban UBANGIJI, a gaban labulen wuri mai tsarki. [7] Sa’an nan firist
ɗin zai zuba jinin a ƙahonin bagaden turare masu ƙanshi da suke a gaban UBANGIJI
a Tentin Sujada. Sauran jinin bijimin zai zuba a gindin bagaden hadaya ta ƙonawa a
ƙofar zuwa Tentin Sujada. [8] Zai cire dukan kitsen daga bijimin hadaya don zunubi,
kitsen da ya rufe kayan cikin, ko kuwa da suka shafe su, [9] da ƙodoji biyu tare da
kitsen da yake kansu kusa da kwiɓi, da kuma murfin hanta, waɗanda zai cire tare
da ƙodoji. [10] Zai cire su daidai kamar yadda akan cire na bijimin hadaya ta salama.
Sai firist ɗin yă ƙone su a kan bagaden ƙona hadaya. [11] Amma fatar ɗan bijimin,
da namansa, da kansa, da ƙafafunsa, da kayan cikinsa, da hanjinsa, [12] wato, dukan
sauran bijimi, dole yă ɗauke su zuwa waje da sansani zuwa wani wuri mai tsabta
inda ake zub da toka, yă ƙone shi a itacen da yake cin wuta a tarin toka.

[13] “ ‘In dukan jama’ar Isra’ilawa suka yi zunubi ba da gangan ba, har suka aikata
ɗaya daga cikin abubuwan da UBANGIJI ya umarta kada a yi, ko da yake jama’ar ba
su san batun ba, duk da haka sun yi laifi. [14] Sa’ad da suka gane da zunubin da suka
aikata, dole taron su kawo ɗan bijimi a matsayin hadaya don zunubi, su kawo shi a
gaban Tentin Sujada. [15] Dattawan jama’a za su ɗibiya hannuwansu a kan bijimin a
gaban UBANGIJI, sai a yanka bijimin a gaban UBANGIJI. [16] Sa’an nan shafaffen firist zai
ɗibi jinin bijimi zuwa cikin Tentin Sujada. [17] Zai tsoma yatsarsa cikin jini yă kuma
yayyafa shi a gaban UBANGIJI sau bakwai a gaban labule. [18] Zai zuba jinin a ƙahonin
bagaden da suke gaban UBANGIJI a cikin Tentin Sujada. Zai zuba sauran jinin a gindin
bagaden hadaya ta ƙonawa a ƙofar zuwa Tentin Sujada. [19] Zai cire dukan kitsen daga
gare shi yă ƙone a kan bagade, [20] yă kuma yi da wannan bijimi kamar yadda ya yi da
bijimi na hadaya don zunubi. Ta haka firist zai yi kafara dominsu, za a kuwa gafarta
musu. [21] Sa’an nan zai ɗauki bijimin waje da sansani yă ƙone shi kamar yadda ya
ƙone bijimi na fari. Wannan ita ce hadaya don zunubi domin jama’a.

[22] “ ‘Sa’ad da shugaba ya yi zunubi ba da gangan ba, har ya aikata ɗaya daga cikin
abubuwan da UBANGIJI Allahnsa ya umarta, to, ya yi laifi. [23] Sa’ad da aka sanar da shi
game da zunubin da ya yi, dole yă kawo bunsuru marar lahani a matsayin hadayarsa.
[24] Zai ɗibiya hannunsa a kan bunsurun yă kuma yanka shi a inda ake yankan hadayar
ƙonawa a gaban UBANGIJI. Hadaya ce ta zunubi. [25] Sa’an nan firist zai ɗibi jinin
hadaya don zunubi da yatsarsa yă sa a ƙahonin bagaden hadayar ƙonawa, yă kuma
zuba sauran jinin a gindin bagade. [26] Zai ƙone dukan kitse a kan bagade kamar
yadda ya ƙone kitsen hadaya ta salama. Ta haka firist zai yi kafara saboda zunubin
mutumin, za a kuwa gafarta masa.

[27] “ ‘In wani memba a cikin jama’a ya yi zunubi ba da gangan ba, ya aikata ɗaya
daga cikin abubuwan da UBANGIJI ya umarta kada a yi, to, ya yi laifi. [28] Sa’ad da aka

sanar da shi game da zunubin da ya yi, dole yă kawo akuya marar lahani a matsayin
hadayarsa domin zunubin da ya yi. 29 Zai ɗibiya hannunsa a kan hadaya don zunubin
yă kuma yanka ta a inda ake hadaya ta ƙonawa. 30 Sa'an nan firist zai ɗibi jinin da
yatsarsa yă zuba a ƙahoni a bagaden hadaya ta ƙonawa, yă kuma zuba sauran jinin
a ƙasan bagade. 31 Za a ɗebe kitsenta duka kamar yadda akan ɗebe kitsen hadaya ta
salama. Firist zai ƙona shi a kan bagaden don ƙanshi mai daɗi ga UBANGIJI. Ta haka
firist zai yi kafara dominsa, za a kuwa gafarta masa.

32 " 'Idan kuwa daga cikin 'yan tumaki zai ba da hadayarsa, sai ya kawo 'yar tunkiya
marar lahani. 33 Zai ɗibiya hannunsa a kanta yă kuma yanka ta hadaya don zunubi
a inda ake yankan hadayar ƙonawa. 34 Sa'an nan firist zai ɗibi jinin hadaya don
zunubin da yatsarsa yă zuba a ƙahonin bagaden hadayar ƙonawa, yă kuma zuba
sauran jinin a gindin bagade. 35 Zai kuma ɗebe kitsenta duka kamar yadda a kan
ɗebe na ragon hadaya ta salama. Firist zai ƙone shi a bisa bagaden a bisa hadaya ta
ƙonawa ga UBANGIJI. Ta haka firist ɗin zai yi kafara dominsa saboda zunubin da ya
yi, za a kuwa gafarta masa.

# 5

1 " 'Mutum zai yi zunubi in bai yi magana ba sa'ad da ya ji ana shelar neman shaida
game da wani abin da ya gani ko kuwa ya ji, alhakin zai zauna a wuyansa.

2 " 'Ko kuwa in mutum ya taɓa wani abin da yake mai ƙazanta, ko gawar naman
jeji marar tsabta, ko na shanu marar tsabta, ko na halittu marasa tsabtan da suke
motsi a ƙasa; ko da yake bai sani ba, ya ƙazantu ke nan, kuma ya yi laifi. 3 Ko kuwa
in ya taɓa rashin tsabta na mutane, wani abin da zai sa shi rashin tsabta; ko da yake
bai sani ba, sa'ad da ya gane, zai zama mai laifi. 4 Ko kuwa in mutum bai yi tunani
ba, ya yi rantsuwar yin wani abu, ko mai kyau ko marar kyau; ko da yake bai sani
ba, duk da haka sa'ad da ya gane zai zama mai laifi. 5 Sa'ad da wani yana da laifi a
kowanne cikin waɗannan hanyoyi, dole yă furta a hanyar da ya yi zunubin 6 kuma
don zunubin da ya yi, dole yă kawo wa UBANGIJI tunkiya ko akuya daga garke kamar
hadaya don zunubi; firist kuwa zai yi kafara dominsa da kuma domin zunubinsa.

7 " 'In ba zai iya kawo tunkiyar ba, sai yă kawo kurciyoyi biyu ko tattabarai biyu
ga UBANGIJI a matsayin hakki don zunubinsa, ɗaya domin hadaya don zunubi ɗayan
kuma domin hadaya ta ƙonawa. 8 Zai kawo su wa firist, wanda da fari zai miƙa
ɗaya domin hadaya don zunubi. Zai murɗe kan daga wuyanta, ba tare da tsinke kan
gaba ɗaya ba, 9 zai kuma yayyafa jinin hadaya don zunubin a gefen bagade; a tsiyaye
sauran jinin kuma a gindin bagade. Hadaya ce ta zunubi. 10 Firist zai miƙa ɗayan
matsayin hadaya ta ƙonawa bisa ga yadda aka tsara, yă kuma yi kafara dominsa
saboda zunubin da ya yi, za a kuwa gafarta masa.

11 " 'In ba zai iya kawo kurciyoyi biyu ko tattabarai biyu ba, sai yă kawo humushin
garwan* gari mai laushi domin hadaya don zunubi. Ba lalle ba ne yă sa mai ko turare
a kansa, saboda wannan hadaya ce ta zunubi. 12 Zai kawo wa firist, firist kuwa zai
ɗiba da hannu don yă kasance abin tunawa, sai yă ƙone a bisan bagaden kamar
hadayar da ake ƙona da wuta ga UBANGIJI. Hadaya ce ta zunubi. 13 Ta haka firist
zai yi kafara dominsa saboda dukan waɗannan zunuban da ya yi, za a kuwa gafarta
masa. Sauran hadayar za tă zama ta firist, kamar yadda yake bisa ga hadaya ta gari.' "

### *Hadaya ta laifi*
### *(Firistoci 7.1-10)*

14 UBANGIJI ya ce wa Musa, 15 "Sa'ad da mutum ya ci amana, ya kuma yi zunubi
ba da gangan ba dangane da wani cikin abubuwa masu tsarki na UBANGIJI, zai kawo

* **5:11** Wato, mai yiwuwa kamar kwata 2 (kamar lita 2)

ga UBANGIJI rago daga garke wanda ba shi da lahani saboda yin hadaya don laifinsa.
Za a kimata kuɗinsa bisa ga ma'aunin shekel na tsattsarkan wuri. Hadaya ce ta laifi.
16 Dole yă biya abin da ya kāsa yi dangane da abubuwa masu tsarki, yă ƙara kashi
ɗaya bisa biyar na darajar abin a kan wannan sa'an nan yă ba wa firist. Firist kuwa
zai yi kafara dominsa da ragon hadaya don laifi. Za a kuwa gafarta masa.
17 "In mutum ya yi zunubi, ya aikata ɗaya daga cikin abubuwan da UBANGIJI ya
umarta kada a yi, ko da yake bai sani ba, shi mai laifi ne. Za a kuwa nemi hakki daga
gare shi. 18 Zai kawo wa firist rago daga garke, marar lahani. Za a kimanta tamanin
rago daidai da tamanin hadaya don laifi. Firist kuwa zai yi kafara don kuskuren da
mutumin ya yi ba da saninsa ba, za a gafarta masa. 19 Hadaya ce ta laifi, ya yi laifi
na† abin da ya yi marar kyau ga UBANGIJI."

# 6

*(Kidaya 5.5-10)*
1 UBANGIJI ya ce wa Musa, 2 "In wani ya yi zunubi bai kuma yi aminci ga UBANGIJI
ba, wato, ta wurin yin wa abokin zamansa karya game da ajiyar da abokin ya ba shi
amana, ko a kan wani alkawarin da suka yi wa juna, ko kuwa a kan yă cuci abokin,
3 ko kuma idan ya sami abin da ya ɓace amma ya yi ƙarya cewa bai samu ba. Ko
ya yi rantsuwar ƙarya a kan duk irin abubuwan da akan aikata na laifi, 4 sa'ad da
mutum ya yi irin laifin nan, ya kuwa tabbata mai laifi ne, to, sai yă komar da abin
da ya ƙwace, ko abin da ya samu ta hanyar zalunci, ko abin da aka ba shi ajiya, ko
abin da ya tsinta. 5 Zai mai da abin da ya yi rantsuwar ƙarya a kai. Zai mayar wa
mai abin da abinsa a yadda yake, har yă ƙara kashi ashirin bisa ɗari na abin. A
ranar da zai yi hadaya don laifinsa, a ranar ce zai mayar wa mai abin da abinsa. 6 A
matsayin hakki kuwa, dole yă kawo wa firist, wato, ga UBANGIJI, hadaya rago marar
lahani kuma wanda aka kimanta tamaninsa daga garke don laifinsa. 7 Ta haka firist
zai yi kafara dominsa a gaban UBANGIJI, za a kuwa gafarta masa irin laifin da ya yi."

*Hadaya ta ƙonawa*
*(Fitowa 29.38-43; Kidaya 28.1-8)*
8 UBANGIJI ya ce wa Musa, 9 "Ka ba Haruna da 'ya'yansa maza wannan umarni,
'Waɗannan su ne ƙa'idodi don hadaya ta ƙonawa. Hadaya ta ƙonawa za tă kasance
a bagade dukan dare, sai da safe, kuma dole a bar wutar tă yi ta ci a bisa bagaden.
10 Sa'an nan firist zai sa rigunarsa ta lilin da kuma rigar lilin da ake sa a ciki, sa'an
nan yă kwashe tokan hadaya ta ƙonawa da wuta da ta ci a kan bagaden, yă sa kusa
da bagaden. 11 Sa'an nan yă tuɓe waɗannan rigunan yă sa waɗansu, sa'an nan yă
ɗauki tokar yă kai waje da sansani zuwa inda yake da tsabta. 12 Dole a bar wutar da
take bisa bagaden tă yi ta ci; kada tă mutu. Kowace safiya firist zai ƙara itacen wuta,
yă shirya hadaya ta ƙonawa a bisa wutar yă kuma ƙone kitsen hadaya ta salama a
kansa. 13 Dole a bar wutar tă ci gaba da ci a bisa bagade; kada tă mutu.

*Hadaya ta gari*
14 " 'Waɗannan su ne ƙa'idodi domin hadaya ta gari. 'Ya'yan Haruna za su kawo
ta a gaban UBANGIJI, a gaban bagaden. 15 Firist zai ɗiba garin hadayar mai laushin
wanda aka zuba masa mai da kuma turare cike da tafin hannu. Zai ƙona wannan
a bisa bagaden, hadaya ce mai daɗin ƙanshi ga UBANGIJI don tunawa. 16 Haruna da
'ya'yansa maza za su ci sauran, amma za a ci shi ba tare da yisti ba a tsattsarkan
wuri; za su ci shi a harabar Tentin Sujada. 17 Ba za a toya shi da yisti ba; na ba su yă
zama rabonsu daga cikin hadayun da ake ƙonawa da wuta, abu ne mafi tsarki, kamar
hadaya don zunubi da laifi. 18 Kowane ɗa namiji cikin zuriyar Haruna zai iya cinsa.

† **5:19** Ko kuwa ya yi cikakkiyar kafara saboda nasa

Wannan rabonsa ne na kullum na hadayar da aka yi ga Ubangiji da wuta. Wannan
madawwamiyar doka ce cikin zamananku duka. Duk abin da ya taɓa hadayun zai
tsarkaka.' "*
19 Ubangiji ya kuma ce wa Musa, 20 "Wannan ne hadayar da Haruna da 'ya'yansa
maza za su kawo ga Ubangiji a ranar da za a naɗa su firistoci,† humushin garwan
gari mai laushi a matsayin hadaya ta gari na kullum, rabinsa da safe, rabinsa kuma
da yamma. 21 A shirya shi da mai a kwanon tuya, a kawo shi kwaɓaɓɓe sosai, a
miƙa shi hadaya ta gari dunƙule-dunƙule‡ don ƙanshi mai daɗi ga Ubangiji. 22 Duk
wanda aka naɗa daga 'ya'yan Haruna yă zama firist a madadinsa, shi ne zai miƙa
wannan hadayar ga Ubangiji. Zai ƙone hadayar ƙurmus. Wannan za tă zama
dawwammamiyar farilla ce har abada. 23 Kowace hadaya ta gari ta firist, za a ƙone
ta ƙurmus, ba za a ci ba."

### *Hadaya ta zunubi*
### *(Firistoci 4.1,2)*

24 Ubangiji ya ce wa Musa, 25 "Faɗa wa Haruna da 'ya'yansa maza, 'Waɗannan
su ne ƙa'idodi domin hadaya don zunubi. Za a yanka hadaya don zunubi a gaban
Ubangiji a inda ake yankan hadaya ta ƙonawa; dole tă kasance mai tsarki. 26 Firist
da ya miƙa ta zai ci, za a ci ta a tsattsarkan wuri, a harabar Tentin Sujada. 27 Duk
abin da ya taɓa wani sashe na naman, zai zama da tsarki, kuma in wani jini ya ɗiga
a riga, dole ka wanke shi a tsattsarkan wuri. 28 Dole a farfashe tukunyar lakar da
aka dafa naman a ciki; amma in an dafa a tukunyar tagulla, sai a kankare tukunyar,
a kuma ɗauraye da ruwa. 29 Kowane namiji a iyalin firistoci zai iya ci; gama abu
ne mafi tsarki. 30 Amma duk wata hadaya don zunubi wadda aka kawo jininta cikin
Tentin Sujada don a yi kafara a Wuri Mai Tsarki, ba za a ci ba. A maimako haka za
a ƙone ta ɗungum.

## 7

### *Hadaya don laifi*
### *(Firistoci 5.14-19)*

1 " 'Waɗannan su ne ƙa'idodi na hadaya don laifi, hadaya ce tsattsarka. 2 Za a
yanka hadaya don laifi a inda ake yanka hadaya ta ƙonawa, za a kuma yayyafa jinin
a kowane gefe na bagade. 3 Za a miƙa kitsen abin hadaya duka, da wutsiya mai kitse,
da kitsen da yake rufe da kayan ciki, 4 da ƙodoji biyu da kitsen da yake a bisansu
kusa da kwiɓi, da kuma rufin hanta, wanda za a cire tare da ƙodoji. 5 Firist zai ƙone
su a kan bagade, hadaya ce da aka ƙone da wuta ga Ubangiji. Hadaya ce don laifi.
6 Kowane da namiji cikin iyalin firistoci zai iya ci. Sai a tsattsarkan wuri ne za a ci;
gama abu mafi tsarki ne.
7 " 'Hadaya don laifi kamar hadaya don zunubi take, saboda haka ƙa'ida hanyar
yinsu iri ɗaya ce. Su ɗin na firist da ya yi kafara da su ne. 8 Firist da ya miƙa hadaya
ta ƙonawa domin wani, zai iya ajiye fatar wa kansa. 9 Kowace hadaya ta garin da
aka toya a tanda, ko aka dafa a tukunya ko a kan kaskon tuya, na firist da ya miƙa ta
ne, 10 kuma kowace hadaya ta gari wadda aka kwaɓa da mai, ko wadda ba a kwaɓa
ba, ita ma, ta dukan 'ya'ya Haruna ne maza.

### *Hadaya don salama*

11 " 'Waɗannan su ne ƙa'idodin hadaya don zumuncin da mutum zai iya miƙa ga
Ubangiji.

* **6:18** Ko kuwa Duka wanda ya taɓa su dole yă kasance mai tsarki haka ma a aya 27. † **6:20** Ko kuwa kowane
‡ **6:21** Ba a tabbatar da ma'anar Ibraniyanci na wannan kalma ba.

12 “ ‘In ya miƙa hadayar a matsayin hadaya ta godiya ce, to, zai miƙa ta tare da
burodi mai kauri marar yisti, wanda aka kwaɓa da mai, da burodi marar kauri,
wanda aka shafa wa mai, da kuma burodi mai kauri da aka yi da gari mai laushi
wanda aka kwaɓa sosai da mai. 13 Tare da hadayarsa don zumunci ta godiya, zai
miƙa dunƙulen burodin da aka yi da yisti. 14 Zai kuma kawo ɗaya daga kowace a
matsayin hadaya, baiko ne ga Ubangiji. Wannan zai zama na firist da ya yafa jinin
hadaya ta salama ne. 15 Za a ci wannan nama na hadaya don zumunci ta godiya a
ranar da aka miƙa ta, kada yǎ bar wani abu daga naman yǎ kwana.

16 “ ‘In hadayarsa cika wa’adin rantsuwa ce ko kuwa ta yardar rai ce, sai a ci
hadayar a ranar da ya miƙa ta, amma za a iya cin duk abin da ya rage kashegari.
17 Duk naman hadayar da ya rage har kwana uku, dole a ƙone shi. 18 Idan aka ci
naman hadayarsa ta salama a rana ta uku, ba za a karɓi wanda ya ba da hadayar
har ya sami albarkar hadayar ba, naman zai zama abin ƙyama, duk wanda ya ci
kuwa ya yi laifi.

19 “ ‘Ba za a ci naman da ya taɓa wani abu marar tsarki ba; dole a ƙone shi. Game
da sauran nama, kowa da yake mai tsarki zai iya ci. 20 Amma in wani wanda ba shi
da tsarki ya ci naman hadaya ta salama ga Ubangiji, za a fid da mutumin daga cikin
mutanensa. 21 Idan wani mutum ya taɓa abu marar tsarki, ko mutum ne, ko dabba
ce, ko wani abu na banƙyama, ya kuma ci naman hadaya ta salama ga Ubangiji, za
a fid da mutumin daga cikin mutanensa.’ ”

### *An hana cin kitse da kuma jini*

22 Ubangiji ya ce wa Musa, 23 “Ka faɗa wa Isra’ilawa, ‘Kada ku ci wani kitsen shanu,
ko na tumaki, ko kuwa na awaki. 24 Za a iya yin wani amfani da kitsen dabbar da
ta mutu mushe, ko kitsen dabbar da namun jeji su yayyaga, amma kada a kuskura a
ci. 25 Duk wanda ya ci kitsen dabbar da aka miƙa ta wuta ga Ubangiji, za a fid da shi
daga mutanensa. 26 Kuma duk inda kuke zama, ba za ku ci jinin wani tsuntsu ko na
dabba ba. 27 Duk wanda ya ci jini, za a fid da mutumin daga mutanensa.’ ”

### *Rabo don firist*

28 Ubangiji ya ce wa Musa, 29 “Faɗa wa Isra’ilawa, ‘Duk wanda ya kawo hadaya ta
salama ga Ubangiji, sai ya kawo hadayarsa ga Ubangiji daga cikin hadayu na salama.
30 Da hannuwansa zai kawo hadayar da za a ƙona ga Ubangiji; zai kawo kitsen tare da
ƙirjin, yǎ kuma kaɗa ƙirjin a gaban Ubangiji a matsayin hadaya ta kaɗawa. 31 Firist
zai ƙone kitsen a bisa bagade, amma ƙirjin zai zama na Haruna da ’ya’yansa maza.
32 Za ku ba da cinya ta dama ta hadaya don zumuncinku ga firist a matsayin baiko.
33 Ɗan Haruna da ya miƙa jini da kitsen hadaya ta salama, zai ɗauki cinyar tǎ zama
rabonsa. 34 Daga hadaya ta salama ta Isra’ilawa, na ɗauki ƙirjin da aka kaɗa da kuma
cinyar da aka miƙa, na ba da su ga Haruna firist da kuma ’ya’yansa maza a matsayin
rabonsu na kullum daga Isra’ilawa.’ ”

35 Wannan shi ne sashen hadayar da aka ba wa Haruna da ’ya’yansa maza, hadayar
da aka yi ga Ubangiji da wuta, tun ranar da aka gabatar da su don su yi wa
Ubangiji hidima a matsayin firist. 36 A ranar da aka keɓe su, Ubangiji ya umarta
cewa Isra’ilawa su ba da wannan a gare su a matsayin rabonsu na kullum, a dukan
tsararraki masu zuwa.

37 Waɗannan su ne ƙa’idodi don hadaya ta ƙonawa, hadaya ta gari, hadaya don
zunubi, hadaya don laifi, hadaya ta naɗi da kuma hadaya ta salama, 38 waɗanda
Ubangiji ya ba wa Musa a Dutsen Sinai, a Hamadar Sinai, a ranar da ya umarci
Isra’ilawa su kawo hadayunsu ga Ubangiji.

# 8

*Naɗin Haruna da ʼyaʼyansa maza*
*(Fitowa 29.1-37)*
1 UBANGIJI ya ce wa Musa, 2 “Kawo Haruna da ʼyaʼyansa maza, ka ɗauki rigunansu,
man keɓewa, bijimi domin hadaya don zunubi, ʼyan raguna biyu da kuma kwandon
da yake da burodi marar yisti, 3 ka kuma tara dukan jamaʼa a ƙofar Tentin Sujada.”
4 Sai Musa ya yi yadda UBANGIJI ya umarce shi, jamaʼa kuwa suka taru a ƙofar Tentin
Sujada.

5 Sai Musa ya ce wa jamaʼar, “Ga abin da UBANGIJI ya umarta a yi.” 6 Saʼan nan
Musa ya kawo Haruna da ʼyaʼyansa maza gaba, ya kuma wanke su da ruwa. 7 Ya sa
wa Haruna taguwa, ya ɗaura igiya kewaye da shi, ya sa masa riga, ya sa masa efod.
Ya kuma ɗaura masa efod wanda aka yi masa saƙar gwaninta. 8 Ya sa masa ƙyallen
maƙalawa a ƙirji, ya kuma sa Urim da Tummim a ƙyallen maƙalawa a ƙirjin. 9 Sai ya
naɗa masa rawani, daga gaban rawanin ya sa allon zinariya, wato, kambi tsattsarka,
kamar yadda UBANGIJI ya umarce shi.

10 Saʼan nan Musa ya ɗauki man keɓewa ya keɓe tabanakul da kuma kowane abin
da yake cikinsa, ta haka ya tsarkake su. 11 Ya yayyafa mai a kan bagade sau bakwai,
yana keɓe bagade da dukan kayayyaki, da daro, da abin da yake tsaya a kai, don yǎ
tsarkake su. 12 Ya zuba man keɓewa a kan Haruna, ya kuma keɓe shi don yǎ tsarkake
shi. 13 Saʼan nan ya kawo ʼyaʼyan Haruna maza, ya sa musu taguwoyi, ya ɗaɗɗaura
igiyoyi kewaye da su, ya kuma sa musu huluna yadda UBANGIJI ya umarce shi.

14 Saʼan nan ya miƙa bijimi domin hadaya don zunubi, sai Haruna da ʼyaʼyansa
suka ɗibiya hannuwansu a bijimin. 15 Musa ya yanka bijimin ya ɗauki jinin, ya sa
yatsarsa ya zuba a dukan ƙahonin bagade don yǎ tsarkake bagaden. Ya zuba sauran
jinin a gindin bagade. Ta haka ya tsarkake shi don yǎ yi kafara dominsa. 16 Musa
ya ɗebo dukan kitsen da yake kewaye da kayan ciki, da kuma wanda ya rufe hanta,
da ƙodojin, da kuma kitsensu, ya kuma ƙone su a kan bagade. 17 Amma bijimin da
fatarsa da namansa da kuma ƙashinsa ya ƙone su a bayan sansani, yadda UBANGIJI
ya umarce shi.

18 Saʼan nan ya miƙa ɗan rago domin hadaya ta ƙonawa, sai Haruna da ʼyaʼyansa
maza suka ɗibiya hannuwansu a kan ɗan rago. 19 Saʼan nan Musa ya yanka ɗan
ragon, ya kuma yayyafa jinin a kowane gefe na bagaden. 20 Ya yanka ragon gunduwa-
gunduwa ya ƙone kan, ya kuma ƙone gunduwa-gunduwan da kitsen. 21 Ya wanke
kayan cikin da ƙafafun a ruwa, ya kuma ƙone dukan ragon a bisa bagade kamar
hadaya ta ƙonawa, mai daɗin ƙanshi, hadaya ce da aka ƙone da wuta ga UBANGIJI,
yadda UBANGIJI ya umarce shi.

22 Sai ya miƙa ɗayan ɗan ragon, ɗan ragon naɗin, sai Haruna da ʼyaʼyansa maza
suka ɗibiya hannuwansu a kan ɗan ragon. 23 Musa kuwa ya yanka ɗan ragon ya ɗibi
jinin ya sa leɓatun kunnen dama na Haruna, ya kuma sa a babbar yatsarsa ta hannun
dama da kuma a babbar yatsar ƙafarsa ta dama. 24 Musa ya kuma kawo ʼyaʼyan
Haruna gaba, ya sa jini a leɓatun kunnuwansu na dama, ya kuma sa a manyan
yatsotsinsu na hannun dama da kuma a manyan yatsotsinsu na ƙafafunsu na dama.
Saʼan nan ya yayyafa jinin a kowane gefen bagade. 25 Ya ɗibi kitsen, da wutsiya mai
kitse, da kuma dukan kitsen da ke kewaye da kayan ciki, da wanda ya rufe hanta,
ƙodoji biyu da kitsensu da kuma cinya ta dama. 26 Saʼan nan daga cikin kwandon
burodi marar yisti wanda yake a gaban UBANGIJI, ya ɗauko dunƙulen burodi, da
kuma guda da aka yi da mai, da kuma ƙosai; ya sa waɗannan a sassan kitsen, da
kuma a cinya ta dama. 27 Ya sa waɗannan a hannuwan Haruna da ʼyaʼyansa, suka
kuma kaɗa su a gaban UBANGIJI a matsayin hadaya ta kaɗawa. 28 Saʼan nan Musa ya

karɓe su daga hannuwansu ya ƙone a bagade a bisa hadaya ta ƙonawa a matsayin
hadaya ta naɗi, mai daɗin ƙanshi, hadaya ce da aka ƙone da wuta ga UBANGIJI. 29 Ya
kuma ɗauki ƙirjin; rabon Musa na ɗan ragon naɗi, ya kaɗa shi a gaban UBANGIJI, a
matsayin hadaya ta kaɗawa, yadda UBANGIJI ya umarce shi.
30 Sai Musa ya ɗibi man keɓewa da jini daga bagade, ya yayyafa su a kan Haruna
da rigunansa, da kuma a kan 'ya'yansa da rigunansu, don yă tsarkake Haruna da
rigunansa da kuma 'ya'yansa da rigunansu.
31 Sai Musa ya ce wa Haruna da 'ya'yansa maza, "Ku dafa naman a ƙofar Tentin
Sujada, ku kuma ci shi a can tare da burodi daga kwandon naɗi, yadda na umarta,
cewa,* 'Haruna da 'ya'yansa maza za su ci shi.' 32 Sa'an nan ku ƙone sauran naman
da kuma burodin. 33 Kada ku bar ƙofar Tentin Sujada har kwana bakwai, sai ranakun
naɗi suka cika, gama naɗinku zai ɗauki kwana bakwai. 34 Abin da aka yi a yau
umarni ne daga UBANGIJI don yin kafara saboda ku. 35 Dole ku kasance a ƙofar Tentin
Sujada dare da rana har kwana bakwai, ku kuma yi abin da UBANGIJI yake bukata,
don kada ku mutu; gama abin da aka umarce ni ke nan."
36 Saboda haka Haruna da 'ya'yansa maza suka yi kome da UBANGIJI ya umarta ta
wurin Musa.

# 9

*Firistoci sun kama aikinsu*

1 A rana ta takwas, Musa ya kira Haruna da 'ya'yansa maza da kuma dattawan
Isra'ila. 2 Ya ce wa Haruna, "Ka ɗauki ɗan maraƙi domin hadayarka don zunubi da
kuma ɗan rago domin hadaya ta ƙonawa, dukan biyu su kasance marar lahani, ka
miƙa su a gaban UBANGIJI. 3 Sa'an nan ka ce wa Isra'ilawa, 'Ku ɗauki bunsuru na
yin hadaya don zunubi, da ɗan maraƙi bana ɗaya, da ɗan rago bana ɗaya marasa
lahani, don hadaya ta ƙonawa, 4 da bijimi da rago don hadayun salama, a yi hadaya
da su ga UBANGIJI, da hadaya ta gari da aka kwaɓa da mai, gama yau UBANGIJI zai
bayyana a gare ku.' "*
5 Suka ɗauki abubuwan da Musa ya umarta zuwa gaban Tentin Sujada, sai dukan
jama'a suka zo kusa suka tsaya a gaban UBANGIJI. 6 Sa'an nan Musa ya ce, "Ga abin
da UBANGIJI ya umarce ku ku yi, domin ɗaukakar UBANGIJI za tă bayyana gare ku."
7 Musa ya ce wa Haruna, "Matsa kusa da bagaden, ka miƙa hadayarka don zunubi,
da hadayarka ta ƙonawa, ka yi kafara don kanka da kuma don jama'a. Ka kuma
kawo hadayar jama'a, ka yi kafara dominsu kamar yadda UBANGIJI ya umarta."
8 Sai Haruna ya matsa kusa da bagaden, ya yanka ɗan maraƙi na yin hadaya don
zunubi saboda kansa. 9 'Ya'yan Haruna maza suka kawo masa jinin, ya kuma tsoma
yatsarsa a cikin jinin ya zuba cikin ƙahonin bagade; sauran jinin kuwa ya zuba a
gindin bagaden. 10 A kan bagaden, ya ƙone kitsen, ƙodojin, da abin da ya rufe hanta,
daga hadaya don zunubi, yadda UBANGIJI ya umarci Musa. 11 Naman da fatar kuwa
ya ƙone waje da sansanin.
12 Sa'an nan ya yanka hadaya ta ƙonawa. 'Ya'yan Haruna maza suka miƙa masa
jinin, ya kuwa yayyafa shi a kowane gefe na bagaden. 13 Suka miƙa masa hadaya ta
ƙonawa gunduwa-gunduwa, haɗe da kan, ya kuwa ƙone su a bisa bagaden. 14 Sai
ya wanke kayan ciki da ƙafafun, ya kuwa ƙone su tare da hadaya ta ƙonawa a kan
bagade.
15 Sa'an nan Haruna ya kawo hadayar da take domin mutane. Ya ɗauki akuya ta
hadaya don zunubin mutane, ya yanka shi, ya miƙa shi domin hadaya don zunubi
kamar yadda ya yi da na farko.

* **8:31** Ko kuwa aka umarce ni 18 da 19.
* **9:4** Kalmar Ibraniyanci za tă iya haɗa namiji da ta mace; haka ma a ayoyi

16 Ya kawo hadaya ta ƙonawa ya kuma miƙa ta yadda aka tsara. 17 Ya kuma kawo
hadaya ta gari, ya ɗiba a tafi hannu ya ƙone a kan bagade tare da hadaya ta ƙonawa
ta safe.
18 Haruna ya yanka maraƙin da ragon a matsayin hadaya ta salama domin mutane.
'Ya'yansa maza suka miƙa masa jinin, ya kuwa yayyafa shi a kowane gefe na bagade.
19 Amma sashen kitsen maraƙin da na ragon, da wutsiya mai kitse, da kitsen da
yake rufe da kayan ciki, da ƙodoji da kuma kitsen da ya rufe hanta, 20 suka shimfiɗa
waɗannan a kan ƙirjin, sa'an nan Haruna ya ƙone kitsen a kan bagade. 21 Sai Haruna
ya kaɗa ƙirjin da kuma cinyar dama a gaban UBANGIJI a matsayin hadaya ta kaɗawa,
kamar yadda Musa ya umarta.
22 Sa'an nan Haruna ya ɗaga hannuwansa wajen mutane ya sa musu albarka. Da
yake ya miƙa hadaya don zunubi, hadaya ta ƙonawa da kuma hadaya ta salama, sai
ya sauka.
23 Sai Musa da Haruna suka shiga cikin Tentin Sujada. Da suka fita, sai suka sa wa
mutane albarka; sai ɗaukakar UBANGIJI ta bayyana ga dukan mutane. 24 Sai wuta ta
fito daga gaban UBANGIJI ta cinye hadaya ta ƙonawa da sassan kitsen a kan bagaden.
Sa'ad da dukan mutane suka ga haka, sai suka yi ihu suna farin ciki, suka fāɗi rubda
ciki, suka yi sujada.

# 10

*Mutuwar Nadab da Abihu*

1 'Ya'yan Haruna maza, Nadab da Abihu suka ɗauki farantansu, suka sa wuta a
ciki, suka zuba turare a kai; suka kuma miƙa haramtacciyar wuta a gaban UBANGIJI,
ba irin wadda UBANGIJI ya umarta ba. 2 Sai wuta ta fito daga UBANGIJI ta cinye su,
suka kuma mutu a gaban UBANGIJI. 3 Sai Musa ya ce Haruna, "Ga abin da UBANGIJI
yake nufi sa'ad da ya ce,

" 'A cikin waɗanda suka kusace ni
za a tabbata ni mai tsarki ne;
a fuskar dukan mutane
za a kuwa girmama ni.' "

Haruna ya yi shiru.
4 Sai Musa ya kira Mishayel da Elzafan, 'ya'yan Uzziyel kawun Haruna, ya ce musu,
"Ku zo nan; ku ɗauki 'yan'uwanku waje da sansani, daga gaban wuri mai tsarki."
5 Sai suka zo suka ɗauke su, suna nan cikin taguwoyinsu, zuwa waje da sansani yadda
Musa ya umarta.
6 Sa'an nan Musa ya ce wa Haruna da Eleyazar da Itamar 'ya'yansa maza, "Kada
ku bar gashin kanku barkatai,* kada kuma ku yage tufafinku, don kada ku mutu. Yin
haka zai jawo fushin UBANGIJI a kan dukan jama'a. Amma dangoginku, wato, dukan
Isra'ilawa, suna iya kuka saboda waɗanda UBANGIJI ya hallaka da wuta. 7 Kada ku
bar ƙofar Tentin Sujada ko kuwa ku mutu, domin man Shafan UBANGIJI yana kanku."
Saboda haka suka yi kamar yadda Musa ya faɗa.
8 Sa'an nan UBANGIJI ya yi magana da Haruna ya ce, 9 "Kai da 'ya'yanka maza, ba za
ku sha ruwan inabi ko wani abu mai sa jiri ba a duk sa'ad da za ku shiga cikin Tentin
Sujada, in ba haka ba za ku mutu. Wannan dawwammamiyar farilla ce wa tsararraki
masu zuwa. 10 Dole ku bambanta tsakanin mai tsarki da marar tsarki, tsakanin marar
tsabta da mai tsabta, 11 za ku kuma koyar da Isra'ilawa dukan farillan da UBANGIJI ya
ba su ta wurin Musa."
12 Musa ya ce wa Haruna da Eleyazar da Itamar 'ya'yansa maza da suka ragu, "Ku
ɗauki ragowar hadaya ta gari wadda aka yi hadaya ta ƙonawa da ita ga UBANGIJI ku

* **10:6** Ko kuwa Kada ku buɗe kawunanku

ci ba tare da yisti ba, a gefen bagaden, gama tsattsarka ne. 13 Ku ci shi a tsattsarkan
wuri, gama rabonka ne da na ʼyaʼyanka daga cikin hadayun da akan ƙone da wuta
ga UBANGIJI; gama haka aka umarce ni. 14 Amma kai da ʼyaʼyanka maza da mata za
su iya ci ƙirjin da aka kaɗa, da kuma cinyar da aka miƙa. Ku ci su a wuri mai tsabta;
an ba da su gare ku da kuma ʼyaʼyanku a matsayin rabo daga hadaya ta salama ta
Israʼilawa. 15 Cinyar da aka miƙa da kuma ƙirjin da aka kaɗa, dole a kawo su tare
da ɓangarori kitsen hadayun da aka yi ta wuri wuta, don a kaɗa a gaban UBANGIJI a
matsayin hadaya ta kaɗawa. Wannan zai zama na kullayaumi gare ka da ʼyaʼyanka,
yadda UBANGIJI ya umarta."
16 Saʼad da Musa ya nemi sani game da akuyar hadaya don zunubi, ya kuwa gane
cewa an ƙone shi, sai ya yi fushi da Eleyazar da kuma Itamar, ʼyaʼyan Haruna maza
da suka ragu, ya kuma yi tambaya, 17 "Me ya sa ba ku ci hadaya don zunubi a cikin
wuri mai tsarki ba? Mafi tsaki ne; an ba ku ne don a ɗauke laifin jamaʼa ta wurin
yin kafara saboda su a gaban UBANGIJI. 18 Da yake ba a kai jininsa cikin wuri mai
tsarki ba, ya kamata ku ci akuyar a wuri mai tsarki, kamar yadda na umarta."
19 Sai Haruna ya amsa wa Musa, "Yau sun miƙa hadayarsu don zunubi da kuma
hadayarsu ta ƙonawa a gaban UBANGIJI, ga kuma irin waɗannan abubuwa da suka
same ni, da a ce na ci hadaya don zunubi yau, da zai yi kyau ke nan a gaban UBANGIJI?"
20 Da Musa ya ji haka, sai ya gamsu.

# 11

*Abinci mai tsabta da marar tsabta*
*(Maimaitawar Shariʼa 14.3-21)*

1 UBANGIJI ya ce wa Musa da Haruna, 2 "Ku ce wa Israʼilawa, ʻCikin dabbobin da
suke a doron ƙasa, waɗannan ne za ku ci. 3 Za ku iya cin dabbobin da suke da
rababben kofato, waɗanda suke kuma tuƙa.
4 " ʻAkwai waɗanda suke tuƙa ko kuwa suna da rababben kofato kawai, duk da
haka ba za ku ci su ba. Waɗannan kuwa su ne, raƙumi, ko da yake yana tuƙa, amma
ba shi da rababben kofato; saboda haka cin namansa haram ne gare ku. 5 Rema, ko da
yake tana tuƙa, duk da haka ba ta da rababben kofato; saboda haka namanta haram
ne gare ku. 6 Zomo, ko da yake yana tuƙa, duk da haka ba shi da rababben kofato;
saboda haka namansa haram ne gare ku. 7 Alade, ko da yake yana da rababben
kofato, amma ba ya tuƙa, saboda haka namansa haram ne gare ku. 8 Ba za ku ci
namansu ba, ko ku taɓa gawawwakinsu, gama haram ne gare ku.
9 " ʻCikin dukan halittu masu rai da suke a cikin ruwan tekuna da rafuffuka, za ku
iya cin kowane da yake da ƙege da kamɓori. 10 Amma kowace halittar da take cikin
tekuna da koguna da ba ta da ƙege da kamɓori, ko cikin dukan abubuwa masu rai
a ruwa ko kuma sauran halittu a cikin ruwa za ku ɗauka su marasa tsaki ne gare
ku. 11 Da yake abubuwan ƙyama ne a gare ku, ba za ku ci namansu ba, kuma dole
ku yi ƙyamar gawawwakinsu. 12 Duk abin da yake a ruwa amma ba shi da ƙege ko
kamɓori, za ku yi ƙyamarsa.
13 " ʻWaɗannan su ne tsuntsayen da za ku yi ƙyamarsu, ba za ku ci su ba domin sun
zama abin ƙyama. Tsuntsayen kuwa su ne, gaggafa, ungulu, baƙin ungulu, 14 shirwa,
da duk wani irin baƙin shirwa, 15 kowane irin hankaka, 16 mujiya mai ƙaho, jimina,
shaho, da kowane irin shaho, 17 ƙaramin ƙururu, babba da jaka, zalɓe, 18 kazar ruwa,
kwasakwasa, da ungulu, 19 shamuwa, kowane irin jinjimi, katutu da kuma jamage.*
20 " ʻDukan ƙwarin da suke da fikafikai masu tafiya da ƙafafu huɗu abin ƙyama ne
gare ku. 21 Sai dai akwai ƙwarin da suke da fikafikai masu tafiya da ƙafafu huɗu da

* **11:19** Cikakkun sunayen waɗansu tsuntsaye, ƙwari da dabbobi a wannan sura ba tabbatattu ba ne.

za ku ci; waɗanda suke da cinyoyin da suke sa su iya tsalle. 22 Za ku iya cin kowane
irin fāra, gyare, ƙwanso da danginsu. 23 Amma sauran ƙananan ƙwari duka masu
fikafikai, suna kuma jan ciki, abin ƙyama ne a gare ku.

24 " 'Duk wanda ya taɓa mushen waɗannan dabbobi, zai ƙazantu har fāɗuwar rana.
25 Duk wanda ya ɗauki ɗaya daga cikin gawawwakinsu dole yǎ wanke rigunansa, zai
kuma ƙazantu har zuwa yamma.

26 " 'Kowace dabbar da ba ta da rababben kofato ko ba ta tuƙa, haram ce gare ku;
duk wanda ya taɓa gawarsu zai ƙazantu. 27 Duk abin da yake tafiya a kan dāginsa
cikin dabbobin da suke da ƙafa huɗu, haram ne a gare ku. Duk wanda ya taɓa
mushensu zai ƙazantu har zuwa yamma. 28 Duk wanda ya ɗauki gawawwakinsu
dole yǎ wanke rigunansa, zai kuma ƙazantu har yamma. Waɗannan dabbobi za su
zama marasa tsabta a gare ku.

29 " 'Waɗannan ƙananan dabbobi da suke rarrafe a ƙasa, haram ne a gare ku, wato,
murɗiya, da ɓera, da gafiya da irinsa, 30 da tsaka, da hawainiya, da ƙadangare, da
guza, da damo. 31 Dukan waɗanda suke rarrafe, za su zama marasa tsarki gare ku.
Duk wanda ya taɓa su sa'ad da suka mutu, zai zama ƙazantacce har zuwa yamma.
32 Duk abin da mushensu ya fāɗa a kai, zai ƙazantu. Ko a kan itace ne, ko a bisa
tufafi, ko a fata, ko a buhu, ko cikin kowane irin abu da ake amfani da shi, to, tilas
a sa shi cikin ruwa, zai zama ƙazantacce har zuwa yamma, sa'an nan zai tsarkaka.
33 In waninsu ya fāɗi a cikin tukunyar laka, kome da yake a tukunyar zai ƙazantu,
kuma dole a fashe tukunyar. 34 Duk abincin da aka yarda a ci, wanda ya taɓa ruwa
daga irin tukunyan nan zai zama marar tsabta, kuma duk ruwan da za a sha daga
irin tukunyan nan ƙazantacce ne. 35 Kowane irin abu da mushensu ya fāɗa a kai
ya ƙazantu ke nan; ko a kan murhu, ko a tukunyar dahuwa, dole a farfashe su. Su
haramtattu ne kuma dole ku ɗauke su haramtattu. 36 Maɓuɓɓuga ko tafki na tarin
ruwa zai ci gaba da zauna mai tsabta, amma duk wanda ya taɓa ɗaya daga cikin
waɗannan gawawwakin ya haramtu. 37 In gawa ta fāɗi a irin da za a shuka, irin zai
ci gaba da zama mai tsabta. 38 Amma in an sa ruwa a irin sai kuma gawar ta fāɗi a
kai, to, irin ya zama haram gare ku.

39 " 'In dabbar aka yarda a ci ta mutu, duk wanda ya taɓa gawarta zai ƙazantu har
yamma. 40 Duk wanda ya ci wani sashe na gawar dole yǎ wanke rigunansa, kuma
zai ƙazantu har yamma. Duk wanda ya ɗauki gawar dole yǎ wanke rigunansa, zai
kuwa ƙazantu har yamma.

41 " 'Duk dabba mai rarrafe a ƙasa abin ƙyama ne; ba kuwa za a ci shi ba. 42 Ba za
ku ci wani halittar da take rarrafe a ƙasa, ko tana jan ciki, ko tana tafiya a kan ƙafafu
huɗu, ko a kan ƙafafu da yawa ba; abin ƙyama ne. 43 Kada ku ƙazantar da kanku
ta wurin wani daga waɗannan halittu. Kada ku ƙazantar da kanku ta dalilinsu, ko a
mai da ku haramtattu ta wurinsu. 44 Ni ne UBANGIJI Allahnku; ku tsarkake kanku ku
kuma zama da tsarki, domin Ni mai tsarki ne. Kada ku ƙazantar da kanku ta wurin
wani halittar da take rarrafe a ƙasa. 45 Ni ne UBANGIJI wanda ya fitar da ku daga
Masar don in zama Allahnku; saboda haka ku zama da tsarki, domin Ni mai tsarki
ne.

46 " 'Waɗannan ne ƙa'idodi game da dabbobi, tsuntsaye, da kowane abu mai rai
da yake motsi a cikin ruwa, da kowace halitta mai rarrafe a ƙasa. 47 Dole ku
bambanta tsakanin haramtacce da halaltacce, tsakanin halittu masu ran da za a iya
ci da waɗanda ba za a iya ci ba.' "

# 12

*Tsabtaccewa bayan haihuwa*

1 UBANGIJI ya ce wa Musa, 2 “Faɗa wa Isra’ilawa, ‘Macen da ta yi ciki ta kuma
haihu ɗa namiji za tă ƙazantu kwana bakwai, kamar yadda takan ƙazantu a lokacin
al’adarta. 3 A rana ta takwas, za a yi wa yaron kaciya. 4 Sa’an nan dole macen ta jira
kwana talatin don a tsabtacce ta daga zub da jini. Ba za tă taɓa wani abu mai tsarki,
ko ta je wuri mai tsarki ba sai kwanakin tsabtaccewarta sun cika. 5 In ta haifi ’ya
ta mace ce, makoni biyu macen za tă ƙazantu kamar yadda takan kasance a lokacin
al’adarta. Sa’an nan dole tă jira kwana sittin don a tsabtacce ta daga zub da jininta.
6 “ ‘Sa’ad da kwanakin tsabtaccewarta don ɗa namiji ko ’ya ta mace suka cika, sai
ta kawo ɗan rago bana ɗaya wa firist a bakin ƙofar Tentin Sujada don hadaya ta
ƙonawa da tattabara ko kurciya na hadaya don zunubi. 7 Firist zai miƙa su a gaban
UBANGIJI don yă yi kafara dominta, sa’an nan tă tsabtacce daga zub da jininta.
“ ‘Waɗannan su ne ƙa’idodi domin macen da ta haifi ɗa namiji ko ’ya ta mace. 8 In
ba za tă iya kawo ɗan rago ba, sai ta kawo kurciyoyi biyu ko tattabarai biyu, ɗaya
domin hadaya ta ƙonawa ɗayan kuma domin hadaya don zunubi. Ta haka firist zai
yi kafara dominta, za tă kuwa zama tsabtacciya.’ ”

# 13

*Ka’idodi game cututtukan fatar jiki*

1 UBANGIJI ya ce wa Musa da Haruna, 2 “Sa’ad da wani yana da kumburi, ko
ɓamɓaroki, ko tabo a fatar jikinsa da zai iya zama cutar fatar jiki,[*] dole a kawo shi
ga Haruna firist, ko kuwa ga ɗaya a cikin ’ya’yansa maza[†] wanda yake firist. 3 Firist
zai bincika mikin da yake a fatar mai cutar, in gashin a mikin ya juya ya zama fari,
mikin kuma ya zama kamar ya fi zurfin fatar jiki, wannan cutar kuturta ce. Sa’ad
da firist ya bincike shi, zai furta shi marar tsarki. 4 In tabon a fata jikinsa fari ne
amma bai zama ya fi zurfin fatar jikin ba, gashin a cikinsa kuma bai juya ya zama
fari ba, firist ɗin zai kaɗaice mai cutar na kwana bakwai. 5 A rana ta bakwai firist
zai bincike shi, in kuwa ya ga cewa mikin bai canja ba, bai kuwa yaɗu a fatar jikin
ba, zai kaɗaice shi na waɗansu ƙarin kwana bakwai. 6 A rana ta bakwai ɗin firist zai
sāke bincike shi, in kuwa mikin ya bushe bai kuwa yaɗu a fatar jikin ba, firist ɗin zai
furta shi mai tsarki; ƙurji ne kawai. Dole mutumin yă wanke rigunansa, zai kuma
tsarkaka. 7 Amma in ƙurjin ya yaɗu a fatar jikinsa bayan ya nuna kansa ga firist don
a furta shi tsarkake, dole yă sāke bayyana a gaban firist. 8 Firist ɗin zai bincike shi,
in ƙurjin ya yaɗu a fatar jikinsa, zai furta shi marar tsarki; cuta ce mai yaɗuwa.
9 “Sa’ad da wani yana da cutar fatar jiki, dole a kawo shi ga firist. 10 Firist zai
bincike shi, in kuwa farin kumburi a fatar jikin ya juyar da gashin fari in kuma
akwai sabon miki a kumburi, 11 to, cutar fatar jikin ne mai ƙarfi kuma firist zai furta
shi marar tsarki. Ba zai kaɗaice shi ba, domin ya riga ya zama marar tsarki.
12 “In cutar ta fashe ko’ina a fatar jiki, har iyakar ganin firist, ta rufe dukan fatar
jikin mai fama da cutar, daga kai har zuwa ƙafa, 13 firist zai bincike shi, in cutar ta
riga ta rufe dukan jikinsa, zai furta wannan mutum tsarkakakke ne. Da yake ya juya
fari fat, tsarkakakke ne. 14 Amma sa’ad da sabon miki ya bayyana a jikinsa, zai furta
shi marar tsarki. 15 Sa’ad da firist ɗin ya ga sabon miki, zai furta shi marar tsarki.
Sabon mikin marar tsarki, yana da cuta mai yaɗuwa. 16 A ce sabon mikin ya canja
ya juya fari, dole yă je wurin firist. 17 Firist zai bincike shi, in kuma mikin ya juya ya
zama fari, firist zai furta mai cutar tsarkakakke; to, zai zama tsarkakakke.
18 “Sa’ad da wani yana da kumburi a fatar jikinsa ya kuma warke, 19 kuma a inda
ƙurjin yake, wani farin kumburi ko tabo ja-ja, fari-fari ya bayyana, dole yă gabatar

[*] **13:2** A al’adance kuturta; an yi amfani da ma’anar kalmar Ibraniyancin nan don cututtuka dabam-dabam da yake shafan fatar jiki, ba lalle kuturta ba; haka ma a ko’ina a cikin wannan sura. [†] **13:2** Ko kuwa zuriya

da kansa ga firist. 20 Firist zai bincike shi, in kuma ya zama ya fi fatar jiki zurfi
kuma gashinsa ya juya ya zama fari, firist ɗin zai furta shi marar tsarki. Cuta ce mai
yaɗuwa da ta fasu a inda ƙurjin yake. 21 Amma in sa'ad da firist ya bincike shi, ya
tarar babu farin gashi a ciki, kuma bai yi zurfi fiye da fatar jikin ba, ya kuma bushe,
sai firist ɗin ya kaɗaice shi har kwana bakwai. 22 In yana yaɗuwa a cikin fatar jikin,
firist zai furta shi marar tsarki; cuta mai yaɗuwa ce. 23 Amma in tabon bai canja ba,
bai kuma yaɗu ba, tabo ne kawai daga ƙurji, kuma firist zai furta shi tsarkakakke.

24 "Sa'ad da wani yana da ƙuna a fatar jikinsa, wurin kuwa ya yi ja-ja, ko fari-fari,
ko kuwa farin tabo ya bayyana a sabon miki na ƙunan, 25 firist zai bincike tabon,
idan kuma gashin a cikinsa ya juya ya zama fari, kuma ya yi zurfi fiye da fatar jikin,
cuta ce mai yaɗuwa da ta fasu daga ƙunan. Firist zai furta shi marar tsarki; cuta
ce mai yaɗuwa. 26 Amma in firist ɗin ya bincike shi bai kuwa ga wani farin gashi a
wurin ba, in kuma bai yi zurfi fiye da fatar jikin ba, ya kuma bushe, to, firist ɗin zai
kaɗaice shi na kwana bakwai. 27 A rana ta bakwai ɗin firist zai bincike shi, in kuma
cutar tana yaɗuwa a cikin fatar jikin, firist ɗin zai furta shi marar tsarki, cutar fatar
jiki ce mai yaɗuwa. 28 In kuma wurin bai canja ba, bai kuma yaɗu cikin fatar jikin
ba amma ya bushe, kumburi ne daga ƙuna, firist ɗin kuwa zai furta shi tsarkakakke;
tabo ne kawai daga ƙuna.

29 "In namiji ko ta mace tana da miki a kai ko kuwa a gemu, 30 firist zai bincike
mikin, in ya yi zurfi fiye da fatar jiki, gashin ya zama rawaya, ya kuma zama siriri,
firist zai furta wannan mutum marar tsarki; ƙaiƙayi ne, cuta mai yaɗuwa ce na kai
ko na gemu. 31 Amma in, sa'ad da firist ya bincika wannan irin mikin, bai yi zurfi
fiye da fatar jiki ba kuma babu baƙin gashi a cikinsa, firist ɗin zai kaɗaice mutum
mai fama da cutar, kwana bakwai. 32 A rana ta bakwai ɗin firist zai bincika mikin in
kuwa ƙaiƙayin bai bazu ba, ba rawayan gashi kuma a ciki, babu zurfin da yake fiye
da fatar jiki, 33 dole a yi masa aski, sai dai ba zai aske wurin cutar ba, kuma firist zai
kaɗaice shi kwana bakwai. 34 A rana ta bakwai firist zai bincike ƙaiƙayin, idan bai
bazu a fatar jikin ba, bai kuma yi zurfin fiye da fatar jikin ba, firist ɗin zai furta shi
tsarkakakke. Dole kuma yǎ wanke rigunansa, zai kuwa zama tsarkakakke. 35 Amma
in ƙaiƙayin ya yaɗu a cikin fatar jikin bayan aka furta shi tsarkakakke, 36 firist ɗin
zai bincike shi, in kuma ƙaiƙayin ya yaɗu a fatar jikin, firist ɗin ba ya bukatar neman
ganin rawayan gashi; mutumin marar tsarki ne. 37 In fa a ganinsa bai canja ba kuma
baƙin gashi ya fito a cikinsa, ƙaiƙayin ya warke ke nan. Mutumin tsarkakakke ne,
firist ɗin kuwa zai furta shi tsarkakakke.

38 "Sa'ad da namiji ko ta mace tana da farare wurare a fatar jiki, 39 firist ya bincika
su, in kuma wuraren toka-toka ne, to, ƙurji marar lahani ne ya faso a fatar jikin;
wannan mutum tsarkakakke.

40 "Mutumin da ya rasa gashi kansa ya zama mai sanƙo ke nan, duk da haka
mutumin tsattsarka ne. 41 In ya rasa gashin goshinsa yana kuma da sanƙo a goshinsa,
shi tsarkakakke ne. 42 Amma in yana da miki ja-ja da ya yi fari a sanƙonsa ko a
goshinsa, cuta mai yaɗuwa ce take fasuwa a kai ko a goshin. 43 Sai firist ya bincike
shi, in kuma kumburarren miki a kansa ko goshinsa ja-ja da fari-fari kamar cutar
fatar jiki mai yaɗuwa ne, 44 mutumin ya kamu da cutar kuma marar tsarki ne. Firist
ɗin zai furta mutumin marar tsarki saboda mikin da yake a kansa.

45 "Mutum mai wannan cuta mai yaɗuwa dole yǎ sa yagaggun riguna, yǎ kuma
bar gashin kansa ba gyara, yǎ rufe sashe ƙasa na fuskarsa, sa'an nan yǎ riga cewa,
'Marar tsarki! Marar tsarki!' 46 Muddin yana da cutar zai ci gaba da kasance marar
tsarki. Dole yǎ yi zama shi kaɗai; dole yǎ yi zama waje da sansani.

### *Ka'idodi game da cutar fatar jiki a riguna*

47 “In akwai cutar fatar jiki a riguna, duk wani rigar ulu ko na lilin, 48 duk wani
kayan zare, ko saƙa na lilin, ko ulu, duk wani kayan fata, ko wanda aka yi da fata,
49 in kuma cutar a cikin rigar, ko fatar, ko kayan saƙan kore-kore ne, ko ja-ja, to, cutar
fatar jiki da ake samu a riguna ce mai yaɗuwa, kuma dole a nuna wa firist. 50 Firist
ɗin zai bincike cutar fatar jikin da take a rigar, yă kuma kaɗaice kayan da abin ya
shafe shi kwana bakwai. 51 A rana ta bakwai ɗin zai bincike shi, in cutar rigar ta
yaɗu, ko a tariyar zaren, ko a wadarin, ko a fatar, ko kuwa a duk abin da ake amfani
da shi, to wannan muguwar cutar riga ce; kayan marar tsarki ne. 52 Dole yă ƙone
rigar, ko tariyar zaren, ko kayan da aka saƙa na ulu ko lilin, ko kuwa na kaya da
aka yi da fatar, wanda cutar ta fāɗa wa, domin cutar rigar muguwa ce, dole a ƙone
kayan.
53 “Amma in sa’ad da firist ya bincike shi, cutar rigar ba ta yaɗu a rigar, ko a tariyar
zare, ko a kayan da aka saƙa, ko a kayan da aka yi da fata ba, 54 zai umarta cewa a
wanke kayan da cutar ta shafa. Sa’an nan zai kaɗaice shi na waɗansu kwana bakwai.
55 Bayan an wanke kayan da cutar ta shafa, firist zai bincike shi, in kuwa cutar rigar
ba tă canja yadda take ba, ko da yake ba tă yaɗu ba, marar tsarki ce. 56 In sa’ad
da firist ya bincike shi, cutar rigar ta bushe bayan da aka wanke kayan, sai yă yage
sashen da cutar ta shafa na rigar, ko fatar, ko tariyar zaren, ko kuwa na kayan da
aka saƙa. 57 Amma in ya sāke bayyana a rigar, ko a tariyar zaren, ko a kayan da aka
saƙa, ko a kayan da aka yi da fatar, to, yana yaɗuwa ke nan, kuma dole a ƙone duk
abin da yake da cutar rigar da wuta. 58 Rigar, ko tariyar zare, ko kayan da aka saƙa,
ko kuwa duk kayan da aka yi da fatar da aka wanke, aka kuma fid da cutar rigar,
dole a sāke wanke shi, zai kuwa zama tsarkakakke.”
59 Waɗannan su ne ƙa’idodi game da cutar fatar jiki na rigar ulu, ko rigar lilin,
tariyar zare, ko kayan da aka saƙa, ko kuwa duk wani abin da aka yi da fata, don
furta su tsarkakakke, ko kuwa marar tsarki.

# 14

*Tsabtaccewa daga cutar fatar jiki mai yaɗuwa*

1 UBANGIJI ya ce wa Musa, 2 “Waɗannan su ne ƙa’idodi domin mutumin da yake da
cuta a lokacin tsabtaccewarsa, sa’ad da aka kawo shi ga firist. 3 Firist zai fita waje da
sansani ya bincike shi. In mutumin ya warke daga cutar fatar jiki mai yaɗuwa, 4 firist
zai umarta a kawo tsuntsaye biyu masu rai, masu tsabta da itacen al’ul, jan ƙyalle
da kuma hizzob saboda mutumin da za a tsabtacce. 5 Sa’an nan firist zai umarta a
kashe ɗaya daga cikin tsuntsayen a bisa ruwa mai kyau a tukunyar laka. 6 Zai ɗauki
tsuntsu mai rai ya tsoma shi tare da itacen al’ul, jan ƙyalle da kuma hizzob cikin jinin
tsuntsun da aka yanka a bisa ruwa mai kyau. 7 Sau bakwai zai yayyafa wa mutumin
da za a tsabtacce daga cutar mai yaɗuwa ya kuma furta shi tsarkakakke. Sa’an nan
ya saki tsuntsu mai rai ɗin ya tafi.
8 “Dole mutumin da aka tsabtaccen ya wanke rigunansa, ya aske dukan gashinsa
ya kuma yi wanka; sa’an nan zai tsabtacce. Bayan wannan zai iya zo cikin sansani,
amma dole yă tsaya waje da tentinsa kwana bakwai. 9 A rana ta bakwai ɗin dole yă
aske dukan gashinsa; dole yă aske kansa, gemunsa, gashin girarsa da sauran gashinsa.
Dole yă wanke rigunansa ya kuma yi wanka, zai kuwa tsabtacce.
10 “A rana ta takwas dole yă kawo ɗan rago da ’yar tunkiya bana ɗaya, kowane
marar lahani, tare da rabin garwan gari mai laushi haɗe da mai domin hadaya ta
gari, da kuma moɗa ɗaya na mai. 11 Firist da ya furta shi tsarkakakke zai miƙa da
wanda za a tsabtaccen da kuma hadayunsa a gaban UBANGIJI a ƙofar Tentin Sujada.
12 “Sa’ad da firist zai ɗauki ɗaya daga cikin ragunan ya kuma miƙa shi kamar
hadaya don laifi, tare da moɗan mai; zai kaɗa su a gaban UBANGIJI kamar hadaya

kaɗawa. 13 Zai yanka ɗan ragon a tsattsarkan wuri inda ake yanka hadaya don
zunubi da hadaya ta ƙonawa. Gama yadda hadaya ta zunubi ta firist ne, haka hadaya
domin laifi ma, hadaya ce mafi tsarki. 14 Firist ɗin zai ɗiba jinin hadaya don laifin
ya zuba a leɓatun kunnen dama na wanda za a tsabtacce, a babbar yatsar hannunsa
na dama a kuma a babbar yatsar ƙafa damansa. 15 Firist ɗin zai ɗiba daga moɗan
mai ɗin ya zuba a tafin hannunsa na hagu, 16 ya tsoma yatsarsa ta dama cikin man
da yake a tafin hannunsa, kuma da yatsar zai yayyafa man a gaban UBANGIJI sau
bakwai. 17 Firist zai sa sauran mai da yake cikin tafinsa a leɓatun kunnen dama na
wanda za a tsabtacce, a babbar yatsarsa na dama da kuma a babbar yatsar ƙafarsa
ta dama, a bisa jinin hadaya don laifin. 18 Sauran man a tafin hannunsa firist zai sa
a kan wanda za a tsabtaccen ya kuma yi kafara dominsa a gaban UBANGIJI.
19 "Sa'an nan firist ɗin zai miƙa hadaya don zunubi ya kuma yi kafara saboda
wannan da za a tsabtacce daga rashin tsarkinsa. Bayan haka, firist zai yanka hadaya
ta ƙonawa 20 ya miƙa ta a bagade, tare da hadaya ta gari, ya kuma yi kafara dominsa,
zai kuwa tsabtacce.
21 "In kuwa mutumin matalauci ne ba zai iya samu waɗannan ba, to, dole yă ɗauki
ɗan rago guda kamar hadaya don laifi a kaɗa don a yi kafara dominsa, tare da
humushin garwa gari mai laushi haɗe da mai don hadaya ta gari, da moɗa na mai,
22 da kurciyoyi biyu ko tattabarai biyu, wanda zai iya samu, ɗaya domin hadaya don
zunubi ɗayan kuma domin hadaya ta ƙonawa.
23 "A rana ta takwas dole yă kawo su domin tsabtaccewarsa ga firist a ƙofar Tentin
Sujada, a gaban UBANGIJI. 24 Firist zai ɗauki ɗan rago na hadaya don laifi tare da
moɗa na mai, ya kaɗa su a gaban UBANGIJI kamar hadaya ta kaɗawa. 25 Zai yanka
ɗan rago domin hadaya don laifi ya kuma ɗibi jinin ya sa a leɓatun kunnen dama na
wanda za a tsabtaccen, a babban yatsar hannun damansa da kuma a babban yatsar
ƙafarsa na dama. 26 Firist zai zuba man a tafin hannunsa na hagu, 27 da yatsarsa
na dama zai yayyafa man daga tafinsa sau bakwai a gaban UBANGIJI. 28 Daga cikin
man da yake a tafinsa zai zuba a wuri da ya zuba jinin hadaya don laifi, a leɓatun
kunnen dama na wanda za a tsabtaccen, a babban yatsar hannun damansa da kuma
a babban yatsar ƙafa damansa. 29 Sauran man da yake cikin tafinsa firist ɗin zai
zuba a kan wannan da za a tsabtaccen don a yi kafara dominsa a gaban UBANGIJI.
30 Sa'an nan zai miƙa kurciyoyi ko tattabarai, waɗanda mutumin zai iya, 31 ɗaya*
kamar hadaya don zunubi ɗayan kuma kamar hadaya ta ƙonawa, tare da hadaya ta
gari. Ta haka firist zai yi kafara a gaban UBANGIJI a madadin wanda za a tsabtacce."
32 Waɗannan su ne ƙa'idodi domin mutumin da yake da cutar fatar jiki wanda
kuma ba zai iya samun abubuwan hadaya ta kullum domin tsabtaccewarsa ba.

### *Tsabtaccewa daga riga mai cutar fatar jiki*

33 UBANGIJI ya ce wa Musa da Haruna, 34 "Sa'ad da kuka shiga ƙasar Kan'ana, wadda
nake ba ku kamar gādonku, na kuma sa yaɗuwa cutar fatar jiki a riga a cikin gida
a wannan ƙasa, 35 dole maigidan ya tafi ya faɗa wa firist ya ce, 'Na ga wani abu
da ya yi kamar cutar fatar jikin da take a riga a cikin gidana.' 36 Firist zai umarci a
fitar da kome a gidan kafin ya shiga ya bincike cutar fatar jiki da take a rigar, saboda
babu abin da yake gidan da za a furta marar tsarki ne. Bayan haka firist zai shiga ya
dudduba gidan. 37 Zai bincike cutar fatar jiki da take a riga a bangaye, in kuma yana
da tabon kore-kore ko ja-ja da suka bayyana da suka yi zurfi fiye da saman bangon,
38 firist ɗin zai fita a bakin ƙofar gidan ya rufe ta na kwana bakwai. 39 A rana ta
bakwai ɗin firist zai dawo don yă dudduba gidan. In cutar fatar jiki da take a riga ta
yaɗu a bangayen, 40 zai umarta a ciccire duwatsun da suke da cutar a zubar a wuri

* **14:31** Seftuwajin da Siriyak; Da Ibraniyanci kamar yadda mutumin zai iya, ɗaya

marar tsarki waje da birnin. 41 Dole yă sa a kankare duka shafen bangon cikin gidan
a kuma zuba kayan da aka kankare a wurin marar tsarki waje da birnin. 42 Sai su
ɗebi waɗansu duwatsu su sa a wuraren da suka ciccire waɗancan, su kuma ɗiba
sabon laka su yi shafen gidan.

43 "In cutar fatar jiki da take ta rigar ta sāke bayyana a gidan bayan an ciccire
duwatsu aka kankare gidan aka kuma yi shafe, 44 firist zai je ya bincika shi, in kuwa
cutar ta bazu a gidan, to, muguwar cuta ce; gidan marar tsarki ne. 45 Dole a rushe
gidan, a fid da duwatsun, katakai da kuma dukan shafen daga birnin zuwa wuri
marar tsarki.

46 "Duk wanda ya shiga gidan yayinda aka rufe shi zai ƙazantu har yamma. 47 Duk
wanda ya kwana ko ya ci abinci a gidan dole yă wanke rigunansa.

48 "Amma in firist ya zo ya bincika gidan kuma cutar fatar jiki da take ta rigar ba tă
bazu ba bayan an yi wa gidan shafe, zai furta gidan tsarkakakke, domin cutar ta tafi.
49 Don a tsabtacce gidan, zai ɗauki tsuntsaye biyu da itacen al'ul, jan ƙyalle da hizzob.
50 Zai yanka ɗaya daga cikin tsuntsayen a bisa ruwa mai kyau a cikin tukunyar laka.
51 Sa'an nan zai ɗauki itacen al'ul, hizzob, jan ƙyalle da kuma tsuntsu mai ran ya
tsoma su cikin jinin tsuntsun da aka yanka da kuma cikin ruwa mai kyau, ya yayyafa
wa gida sau bakwai. 52 Zai tsabtacce gidan da jinin tsuntsun, ruwa mai kyau, tsuntsu
mai ran, itacen al'ul, hizzob da kuma jan ƙyalle. 53 Sa'an nan zai saki tsuntsu mai
rai ɗin a fili waje da birnin ya tafi. Ta haka zai yi kafara saboda gidan, gidan kuwa
zai zama tsarkakakke."

54 Waɗannan su ne ƙa'idodi saboda duk wani cuta mai yaɗuwa, don ƙaiƙayi, 55 don
cutar fatar jiki da take a riga ko a cikin gida, 56 da kuma don kumburi, ɓamɓaroki ko
tabo, 57 don a tabbatar sa'ad da wani abu mai tsarki da marar tsarki.

Waɗannan su ne ƙa'idodi domin cutar fatar jiki mai yaɗuwa da cutar fatar jikin
da take a riga.

# 15

*Mugunyar da ke sa ƙazantuwa*

1 Ubangiji ya ce wa Musa da Haruna, 2 "Yi wa Isra'ilawa magana, ku ce musu, 'Duk
sa'ad da wani namiji yake ɗiga daga azzakarinsa, wannan ɗiga marar tsarki ne. 3 Ko
ɗigar ta ci gaba da fitowa daga azzakarinsa ko an tsere ta, za tă sa mutumin yă zama
marar tsarki. Ga yadda ɗigarsa za tă kawo ƙazantuwa,

4 " 'Duk gadon da mutumin mai ɗigar ya kwanta a kai, zai zama marar tsarki, kuma
duk abin da ya zauna a kai, zai zama marar tsarki. 5 Duk wanda ya taɓa gadonsa
dole yă wanke rigunansa, yă kuma yi wanka, zai kuwa ƙazantu har yamma. 6 Duk
wanda ya zauna a inda wannan mai ɗiga ya zauna a kai, dole yă wanke rigunansa
yă kuma yi wanka, zai kuwa ƙazantu har yamma.

7 " 'Duk wanda ya taɓa jikin mai ɗiga, dole yă wanke rigunansa, yă kuma yi wanka,
zai kuma ƙazantu har yamma.

8 " 'In mai ɗiga ya tofa miyau a kan wani wanda yake tsarkakakke, dole
tsarkakakken nan yă wanke rigunansa, yă kuma yi wanka, zai kuma ƙazantu har
yamma.

9 " 'Kowane sirdi da mai ɗigar ya zauna a kai zai ƙazantu, 10 kuma duk wanda ya
taɓa wani abu cikin abubuwan da suke a ƙarƙashin sirdin zai ƙazantu har yamma;
duk wanda ya ɗauki abubuwan nan dole yă wanke rigunansa, yă kuma yi wanka,
zai kuwa ƙazantu har yamma.

11 " 'Duk wanda mai ɗiga ya taɓa ba tare da ya wanke hannuwansa da ruwa ba,
dole yă wanke rigunansa yă kuma yi wanka, zai kuma ƙazantu har yamma.

12 “ ‘Dole a farfashe tukunya lakar da mutumin ya taɓa, kuma dole a ɗauraye duk
wani abin da aka yi da katako wanda ya taɓa da ruwa.
13 “ ‘Sa’ad da aka tsabtacce mai ɗigar, zai ɗauki kwana bakwai don tsabtaccewarsa;
dole yă wanke rigunansa, yă kuma yi wanka mai tsabta, zai kuwa zama tsarkakakke.
14 A rana ta takwas dole yă ɗauki kurciyoyi biyu ko tattabarai biyu, yă zo gaban
Ubangiji a ƙofar Tentin Sujada, yă ba da su ga firist. 15 Firist ɗin zai miƙa su, ɗaya
domin hadaya don zunubi, ɗayan kuma domin hadaya ta ƙonawa. Ta haka zai yi
kafara a gaban Ubangiji saboda mai ɗigar.
16 “ ‘Sa’ad da namiji ya ɗigar maniyyi, dole yă wanke jikinsa gaba ɗaya da ruwa, zai
kuma ƙazantu har yamma. 17 Dole a wanke duk riga ko fatar da yake da maniyyin a
kansa da ruwa, zai kuma ƙazantu har yamma. 18 Sa’ad da namiji ya kwana da mace
ya kuwa zub da maniyyi, dole dukansu biyu su yi wanka, za su kuma ƙazantu har
yamma.
19 “ ‘Sa’ad mace take al’adarta ta ƙa’ida, rashin tsabtarta ta al’adar zai ɗauki kwana
bakwai, kuma duk wanda ya taɓa ta, zai ƙazantu har yamma.
20 “ ‘Duk abin da ta kwanta a kai a lokacin al’adarta zai ƙazantu, kuma duk abin da
ta zauna a kai zai ƙazantu. 21 Duk wanda ya taɓa gadonta dole yă wanke rigunansa
yă kuma yi wanka, zai kuma ƙazantu har yamma. 22 Duk wanda ya taɓa wani abin
da ta zauna a kai, dole yă wanke rigunansa yă kuma yi wanka, zai kuma ƙazantu
har yamma. 23 Ko gado ne, ko kuwa wani abin da ta zauna a kai, sa’ad da wani ya
taɓa shi, zai ƙazantu har yamma.
24 “ ‘In namiji ya kwana da ita, al’adarta kuwa ta taɓa shi, zai ƙazantu na kwana
bakwai; duk kuma gadon da ya kwanta a kai, zai ƙazantu.
25 “ ‘Idan mace tana ɗigar jini na tsawon kwanaki, ban da kwanakin ganin al’adarta,
ko kuwa idan al’adarta ya wuce yawan kwanakin da ya kamata, to, za tă ƙazantu
daidai kamar na kwanakin al’adar da ta saba yi. Wato, muddin tana cikin ɗiga,
ta zama mai ƙazanta. 26 Duk gadon da ta kwanta yayinda ta ci gaba da ɗiga zai
zama marar tsarki, kamar yadda gadonta yake a lokacin al’adarta, kuma duk abin
da ta zauna a kai zai zama marar tsarki, kamar yadda yake a lokacin al’adarta. 27 Duk
wanda ta taɓa su zai zama marar tsarki; dole yă wanke rigunansa yă kuma yi wanka,
zai kuma ƙazantu har yamma.
28 “ ‘Sa’ad da aka tsabtacce ta daga ɗigarta, dole tă ɗauki kwana bakwai, bayan
haka za tă zama mai tsarki. 29 A rana ta takwas, dole tă ɗauki kurciyoyi biyu ko
tattabari biyu ta kawo su ga firist a bakin ƙofar Tentin Sujada. 30 Firist zai miƙa
ɗaya saboda hadaya don zunubi, ɗayan kuma don hadaya ta ƙonawa. Ta haka zai
yi kafara dominta a gaban Ubangiji saboda ƙazantar ɗigarta.
31 “ ‘Ta haka za ka tsarkake Isra’ilawa daga rashin tsarkinsu, domin kada su
mutu saboda rashin tsarkinsu ta wurin ƙazantar da wurin zamana wanda yake
tsakiyarsu.’ ”
32 Waɗannan su ne ƙa’idodi a kan wanda yake ɗiga, da wanda yake zubar da
maniyyi, 33 ƙa’idodi ne kuma ga mace wadda take al’ada, ga namiji ko macen da take
ɗiga, ga kuma namijin da ya kwana da mace marar tsarki.

# 16

*Ranar kafara*

1 Ubangiji ya yi magana da Musa bayan mutuwar ’ya’yan Haruna biyu maza
waɗanda suka mutu sa’ad da suka kusaci Ubangiji. 2 Ubangiji ya ce wa Musa, “Faɗa
wa ɗan’uwanka Haruna, kada yă riƙa shiga Wuri Mafi Tsarki bayan labule koyaushe,
wato, a gaban murfi wanda yake bisa akwatin alkawari, domin kada yă mutu, gama
zan bayyana a cikin girgije a kan murfin.

3 “Ga yadda Haruna zai shiga wuri mai tsarki, zai zo da ɗan bijimi domin hadaya
don zunubi da kuma rago domin hadaya ta ƙonawa. 4 Zai sa toguwar lilin mai tsarki,
tare da ɗan ciki na lilin; zai yi ɗamara da igiya kewaye da shi, yă kuma sa hular lilin.
Waɗannan su ne riguna masu tsarki; saboda haka dole yă yi wanka kafin yă sa su.
5 Zai ɗauki bunsurai biyu daga jama’ar Isra’ilawa na hadaya don zunubi da ɗan rago
don hadaya ta ƙonawa.

6 “Haruna zai miƙa bijimi hadaya don zunubinsa yă kuma yi kafara don kansa da
gidansa. 7 Sa’an nan zai ɗauki bunsurai biyu yă miƙa su a gaban Ubangiji a ƙofar
Tentin Sujada. 8 Haruna zai jefa ƙuri’a don awaki biyun ɗin, ƙuri’a ɗaya domin
Ubangiji, ɗayan kuma don azazel* 9 Haruna zai kawo akuyar da ƙuri’a ta fāɗi a kai
wa Ubangiji yă miƙa ta na hadaya don zunubi. 10 Amma za a miƙa akuyar da aka
zaɓa ta wurin ƙuri’a a matsayi ta azazel da rai a gaban Ubangiji don a yi amfani da
ita don kafara ta wurin korinta zuwa cikin jeji kamar azazel.

11 “Haruna zai kawo bijimi domin hadayarsa ta zunubi don yă yi kafara wa kansa
da kuma domin gidansa, zai kuma yanka bijimin domin nasa hadaya don zunubi.
12 Zai ɗauki faranti cike da garwashin wuta daga bagade a gaban Ubangiji, yă kuma
cika hannunsa biyu da turare mai ƙanshin da aka niƙa yă kai su bayan labule. 13 Zai
sa turaren a wuta a gaban Ubangiji, hayaƙin turaren kuwa zai rufe murfin kafarar
a bisa Akwatin Alkawari, don kada yă mutu. 14 Zai ɗibi jinin bijimin da yatsarsa yă
yayyafa a gaban murfin kafarar; sa’an nan yă yayyafa jinin da yatsarsa sau bakwai
a gaban murfin kafarar.

15 “Sa’an nan zai yanka akuya na hadaya don zunubi saboda mutane, yă kai jinin
bayan labule, yă yi da shi yadda ya yi da jinin bijimin. Zai yayyafa shi a kan murfin
kafarar da kuma a gabansa. 16 Ta haka zai yi kafara domin Wuri Mafi Tsarki saboda
ƙazantar tawayen Isra’ilawa, da laifofinsu, da dukan zunubansu. Haka zai yi saboda
Tentin Sujada wanda yake a cikinsu a tsakiyar ƙazantarsu. 17 Kada kowa yă kasance
a Tentin Sujada daga lokacin da Haruna ya shiga don yă yi kafara a Wuri Mafi Tsarki
har sai ya fita, bayan ya yi kafara domin kansa, gidansa da kuma dukan jama’ar
Isra’ila.
18 “Sa’an nan zai fita zuwa bagade da yake a gaban Ubangiji, yă yi kafara dominsa.
Zai ɗibi jinin bijimi da na akuya yă zuba a ƙahonin bagade. 19 Zai yayyafa jinin a kan
bagade da yatsarsa sau bakwai, yă tsabtacce shi yă kuma tsarkake shi daga ƙazantar
Isra’ilawa.
20 “Sa’ad da Haruna ya gama yin kafara domin Wuri Mafi Tsarki, Tentin Sujada
da kuma bagade, sai yă kawo akuya mai rai. 21 Haruna zai ɗibiya hannuwansa a
kan akuya mai ran, yă furta a kansa dukan mugunta da tawayen Isra’ilawa, dukan
zunubansu, yă kuma sa su a kan akuyan. Zai kori akuyan zuwa cikin jeji a hannun
mutumin da aka ba shi aikin yin haka. 22 Akuyan zai ɗauka a kansa dukan zunubansu
zuwa kaɗaitaccen wuri, a can mutumin zai sake shi a jeji.

23 “Sa’an nan Haruna zai shiga Tentin Sujada yă tuɓe rigunansa na lilin da ya sa,
kafin yă shiga Wuri Mafi Tsarki, zai kuma bar su a can. 24 Zai yi wanka a tsattsarkan
wuri yă sa rigunarsa na kullum. Sa’an nan zai fita yă miƙa hadaya ta ƙonawa domin
kansa da hadaya ta ƙonawa domin mutane, don yă yi kafara domin kansa da kuma
domin mutane. 25 Zai kuma ƙone kitsen hadaya don zunubi a kan bagade.

26 “Dole mutumin da ya saki akuya na azazel yă wanke rigunansa yă kuma yi
wanka; bayan haka zai iya shiga sansani. 27 Dole a ɗauki jini, fata, nama da kuma
ƙashin bijimi da akuyan hadaya don zunubi, waɗanda aka kawo jininsu cikin Wuri

* **16:8** Wato, akuya don cirewa; Ibraniyanci azazel, haka ma a ayoyi 10 da 26.

Mafi Tsarki don kafara, a kai waje da sansani a ƙone. 28 Dole mutumin da ya ƙone
su yă wanke rigunansa yă kuma yi wanka, bayan haka zai iya shiga sansani.

29 “Wannan za tă zama dawwammamiyar farilla a gare ku. A rana ta goma ga
wata na bakwai, dole ku yi mūsu kanku,† ba kuwa za ku yi wani aiki ba, ko da
mutum baƙo ne a cikinku ko kuwa ɗan ƙasa, 30 gama a wannan rana za a yi kafara
dominku, don a tsarkake ku. Sa’an nan a gaban Ubangiji, za a tsarkake ku daga
dukan zunubanku. 31 Asabbaci ne don hutawa, kuma dole ku yi mūsun kanku;
wannan dawwammamiyar farilla ce. 32 Firist da aka keɓe aka kuma naɗa don yă
gāji mahaifinsa a matsayin babban firist ne zai yi kafara. Zai sa rigunan lilin masu
tsarki 33 yă yi kafara domin Wuri Mafi Tsarki, Tentin Sujada da bagade, da kuma
saboda firistoci da kuma dukan jama’ar Isra’ila.

34 “Wannan za tă zama dawwammamiyar farilla ce gare ku. Za a riƙa yin kafara
sau ɗaya a shekara saboda dukan zunuban Isra’ilawa.”

Aka kuma yi haka, yadda Ubangiji ya umarci Musa.

# 17

### *An hana cin jini*

1 Ubangiji ya ce wa Musa, 2 “Yi magana da Haruna da ’ya’yansa maza da kuma
dukan Isra’ilawa, ka ce musu, ‘Ga abin da Ubangiji ya umarta. 3 Duk mutumin
Isra’ilan da ya yanka sa,* ɗan rago ko akuya a sansani ko waje da shi 4 a maimakon
kawo shi a matsayin hadaya ga Ubangiji a gaban tabanakul na Ubangiji, za a ɗauki
wannan mutum a matsayi mai laifin zub da jini, ya zub da jini, kuma dole a raba
shi da mutanensa. 5 Wannan ya zama haka saboda Isra’ilawa su kawo wa Ubangiji
hadayun da suke yi a filaye. Dole su kawo su ga firist, wato, ga Ubangiji, a ƙofar
Tentin Sujada, su miƙa su a matsayin hadayun salama. 6 Firist zai yayyafa jinin a
bagaden Ubangiji, a ƙofar Tentin Sujada, yă kuma ƙone kitsen kamar ƙanshi mai daɗi
ga Ubangiji. 7 Kada kuma su ƙara yin hadayunsu ga gumaka masu siffar bunsurai
waɗanda suka bauta wa. Wannan za tă zama dawwammamiyar farilla a gare su wa
tsararraki masu zuwa.’

8 “Faɗa musu, ‘Duk wani mutumin Isra’ila ko wani baƙon da yake zama a cikinsu
wanda ya miƙa hadaya ta ƙonawa ko sadaka 9 kuma bai kawo shi a ƙofar Tentin
Sujada don yă miƙa shi ga Ubangiji ba, dole a raba wannan mutum da mutanensa.

10 “ ‘Duk mutumin Isra’ila ko baƙon da yake zama a cikinsu wanda ya ci wani jini,
zan yi gāba da wannan mutum wanda ya ci jinin, za a kuma raba shi da mutanensa.
11 Gama ran halitta yana a cikin jinin, kuma na ba da shi gare ku don kafara a kan
bagade, jini ne yake kafara saboda ran mutum. 12 Saboda haka na ce wa Isra’ilawa,
“Babu waninku da zai ci jini, babu wani baƙon da yake zama a cikinku da zai ci jini.”

13 “ ‘Duk wani mutumin Isra’ila ko baƙon da yake zama a cikinku wanda ya ji wa
wani dabba ko tsuntsu wanda ake ci ciwo, dole yă tsiyaye jinin yă rufe shi da ƙasa,
14 domin ran kowace halitta yana cikin jini. Shi ya sa na ce wa Isra’ilawa, “Kada ku
ci jinin wani halitta, domin ran kowace halitta yana cikin jinin; duk wanda ya ci shi
dole a fid da shi.”

15 “ ‘Kowa, ko haifaffe ɗan ƙasa ko baƙo, da ya ci wani abin da aka sami a mace,
ko naman jeji ya yayyage, dole yă wanke rigunansa, yă kuma yi wanka, zai kuma
ƙazantu har yamma; sa’an nan zai tsarkake. 16 Amma in bai wanke rigunansa ya
kuma yi wanka ba, alhaki zai kasance a kansa.’ ”

---

† **16:29** Ko kuwa dole ku yi azumi; haka ma a aya 31. * **17:3** Kalmar Ibraniyanci ta ƙunshi namiji da ta macen
sa ne.

# 18

*Jima'in da aka hana*

1 UBANGIJI ya ce wa Musa, 2 "Yi wa Isra'ilawa magana ka kuma faɗa musu cewa, 'Ni
ne UBANGIJI Allahnku. 3 Kada ku yi yadda suke yi a Masar inda da kuke zama, kuma
ba a ku yi kamar yadda suke yi a ƙasar Kan'ana inda nake kawo ku ba. Kada ku yi
yadda suke yin abubuwa. 4 Dole ku kiyaye dokokina kuma ku lura ku bi farillaina.
Ni ne UBANGIJI Allahnku. 5 Ku kiyaye farillaina da dokokina, gama mutumin da ya
aikata waɗannan abubuwa zai rayu ta wurinsu. Ni ne UBANGIJI.
6 " 'Kada wani ya kusaci wani dangi na kusa don yǎ yi jima'i. Ni ne UBANGIJI.
7 " 'Kada ka ƙasƙantar da mahaifinka ta wurin kwana da mahaifiyarka. Ita
mahaifiyarka ce; kada ka yi jima'i da ita.
8 " 'Kada ka yi jima'i da matar mahaifinka, wannan zai ƙasƙantar da mahaifinka.
9 " 'Kada ka yi jima'i da 'yar'uwarka, ko 'yar mahaifinka ko 'yar mahaifiyarka, ko
an haife ta a gida ɗaya da kai ko kuwa a wani wuri dabam.
10 " 'Kada ka yi jima'i da 'yar ɗanka ko 'yar 'yarka, wannan zai ƙasƙantar da kai.
11 " 'Kada ka yi jima'i da 'yar matar mahaifinka wadda aka haifa wa mahaifinka;
ita 'yar'uwarka ce.
12 " 'Kada ka yi jima'i da 'yar'uwar mahaifinka, ita dangin mahaifinka ne na kusa.
13 " 'Kada ka yi jima'i da 'yar'uwar mahaifiyarka, domin ita dangin mahaifiyarka
ce na kusa.
14 " 'Kada ka ƙasƙantar da ɗan'uwan mahaifinka ta wurin kusaci matarsa don ka
yi jima'i da ita, ita bābarka ce.
15 " 'Kada ka yi jima'i da matar ɗanka. Ita matar ɗanka ne; kada ka yi jima'i da ita.
16 " 'Kada ka yi jima'i da matar ɗan'uwanka; wannan zai ƙasƙanta ɗan'uwanka.
17 " 'Kada ka yi jima'i da mace da kuma 'yarta. Kada ka yi jima'i da 'yar ɗanta ko
'yar 'yarta; su danginta ne na kusa. Wannan mugun abu ne.
18 " 'Kada ka auri 'yar'uwar matarka ta zama kishiyar matarka ka kuma yi jima'i
da ita yayinda matarka tana da rai.
19 " 'Kada ka kusaci mace don ka yi jima'i da ita a lokacin ƙazantar al'adarta.
20 " 'Kada ka yi jima'i da matar maƙwabcinka ka ƙazantar da kanka tare da ita.
21 " 'Kada ku ba da wani daga cikin 'ya'yanku don a yi hadaya wa* Molek, gama
ba za ku ƙasƙantar da sunan Allahnku ba. Ni ne UBANGIJI.
22 " 'Kada ka kwana da namiji kamar yadda namiji yakan kwana da ta mace,
wannan abin ƙyama ne.
23 " 'Kada ka yi jima'i da dabba ka ƙazantar da kanka. Mace ba za tǎ ba da kanta
ga dabba don yǎ yi jima'i da ita ba; wannan abin ƙyama ne.
24 " 'Kada ku ƙazantar da kanku da wani daga cikin waɗannan, domin haka
al'umman da zan kora a gabanku suka ƙazantu. 25 Har ƙasar ma ta ƙazantu,
saboda haka na hukunta ta saboda zunubinta, ƙasar kuwa ta amayar da mazaunanta.
26 Amma dole ku kiyaye farillaina da kuma dokokina. Kada haifaffe ɗan ƙasa da
baƙin da suke zama a cikinku yǎ yi wani daga cikin waɗannan abubuwa banƙyama,
27 gama mutanen da suka zauna a wannan ƙasa kafin ku sun aikata dukan waɗannan
abubuwa, suka kuma ƙazantu. 28 Kuma in kuka ƙazantar da ƙasar, za tǎ amayar da
ku kamar yadda ta amayar da al'umman da suka riga ku.
29 " 'Duk wanda ya yi wani daga cikin waɗannan abubuwa banƙyama, dole a fid
da mutumin daga cikin mutanensa. 30 Ku kiyaye umarnaina kuma kada yi ku wata
al'ada mai banƙyamar da aka yi kafin ku zo kuma kada ku ƙazantar da kanku da
su. Ni ne UBANGIJI Allahnku.' "

* **18:21** Ko kuwa don a tura cikin wuta

# 19

*Dokoki iri-iri*
1 Ubangiji ya ce wa Musa, 2 “Yi wa taron jama’ar Isra’ila gaba ɗaya magana, ka ce
musu, ‘Ku zama masu tsarki, domin Ni, Ubangiji Allahnku, mai tsarki ne.
3 “ ‘Dole kowannenku yă girmama mahaifiyarsa da mahaifinsa, dole kuma ku
kiyaye Asabbacina. Ni ne Ubangiji Allahnku.
4 “ ‘Kada ku juyo ga gumaka, ko ku yi wa kanku allolin da aka yi zubi da ƙarfe. Ni
ne Ubangiji Allahnku.
5 “ ‘Sa’ad da kuka miƙa hadaya ta salama ga Ubangiji, ku miƙa ta yadda za tă karɓu
a madadinku. 6 Za a ci ta a ranar da kuka miƙa ta, ko kuwa a kashegarin; duk abin da
ya rage har kwana ta uku dole a ƙone shi. 7 In aka ci ta a rana ta uku, marar tsabta ce,
ba kuma za a karɓe ta ba. 8 Duk wanda ya ci ta zai zama da laifi domin ya ƙazantar
da abin da yake da tsarki ga Ubangiji, dole a raba mutumin nan da mutanensa.
9 “ ‘Sa’ad da kuka yi girbin amfanin gonarku, kada ku girbe har zuwa gefen gonar,
ko ku yi kalan girbinku. 10 Kada ku koma gonar inabinku kuna kala, ko ku tattara
’ya’yan inabin da suka fāffāɗi. Ku bar su domin matalauta da kuma baƙi. Ni ne
Ubangiji Allahnku.
11 “ ‘Kada ku yi sata.
“ ‘Kada ku yi ƙarya.
“ ‘Kada ku ruɗe juna.
12 “ ‘Kada ku rantse bisa ƙarya da sunana, ta haka har ku ƙasƙantar da sunan
Allahnku. Ni ne Ubangiji.
13 “ ‘Kada ku zalunci maƙwabcinku, ko ku yi masa ƙwace.
“ ‘Kada ku riƙe albashin ma’aikaci yă kwana.
14 “ ‘Kada ku zagi kurma, ko ku sa abin tuntuɓe a gaban makaho, amma ku ji tsoron
Allahnku. Ni ne Ubangiji.
15 “ ‘Kada ku yi rashin adalci cikin shari’a; kada ku nuna sonkai ga matalauci, ko
ku goyi bayan mai arziki, amma ku shari’anta maƙwabci cikin gaskiya.
16 “ ‘Kada ku yi ta yawo kuna yaɗa ƙarya a cikin mutanenku.
“ ‘Kada ku yi wani abin da zai sa ran maƙwabcinku cikin hatsari. Ni ne Ubangiji.
17 “ ‘Kada ka yi ƙiyayyar ɗan’uwanka a zuciya. Ka tsawata wa maƙwabcinka da
gaske don kada ka sami rabo cikin laifinsa.
18 “ ‘Kada ka nemi yin ramuwa, ko ka riƙe wani cikin mutanenka a zuciya, amma
ka ƙaunaci maƙwabcinka kamar kanka. Ni ne Ubangiji.
19 “ ‘Ku kiyaye farillaina.
“ ‘Kada ku sa dabbobin da ba iri ɗaya ba su yi barbara.
“ ‘Kada ku yi shuki iri biyu a gonarku.
“ ‘Kada ku sa rigar da aka saƙa da yadi iri biyu.
20 “ ‘In wani ya kwana da mace wadda take baiwa, wadda aka yi wa wani alkawari
amma bai fanshe ta ba, ko kuwa ba a ’yantar da ita ba, dole a yi hukuncin da ya dace.
Duk da haka ba za a kashe su ba, domin ba a ’yantar da ita ba. 21 Dole mutumin da ya
kwana da ita yă kawo rago a ƙofar Tentin Sujada domin hadaya don laifi ga Ubangiji.
22 Da ragon hadaya don laifin ne firist zai yi kafara saboda mutumin a gaban Ubangiji
saboda zunubin da ya yi, za a kuwa gafarta zunubinsa.
23 “ ‘Sa’ad da kuka shiga ƙasar kuka kuma shuka kowane irin itace mai ’ya’ya na
ci, ku ɗauki ’ya’yan itatuwan nan a matsayi an hana ku ci.* Shekara uku za ku ɗauka
a matsayi an hana ku, ba za ku ci su ba. 24 A shekara ta huɗu, dukan ’ya’yansu za
su zama tsarkakakku, hadaya ta yabo ga Ubangiji. 25 Amma a shekara ta biyar, za ku
iya cin ’ya’yan itatuwan. Ta haka girbinku zai ƙaru. Ni ne Ubangiji Allahnku.

* **19:23** Da Ibraniyanci marasa kaciya

26 “ ‘Kada ku ci wani abinci tare da jini a cikinsa.
“ ‘Kada ku yi duba ko sihiri.
27 “ ‘Ba za ka aske gefe-gefe na gashin kanka ba, ko ku aske gemunku.
28 “ ‘Kada ku tsattsaga jikunanku saboda matattu, ba kuwa za ku yi wa kanku zāne-zāne a jiki ba. Ni ne UBANGIJI.
29 “ ‘Kada ka ƙasƙantar da ’yarka ta wurin mai da ita karuwa, in ba haka ba ƙasar za tă juya ga karuwanci tă kuma cika da mugunta.
30 “ ‘Ku kiyaye Asabbacina, ku kuma girmama wuri mai tsarkina. Ni ne UBANGIJI.
31 “ ‘Kada ku juya ga masu duba, ko ku nemi shawarar bokaye, gama za ku ƙazantu ta wurinsu. Ni ne UBANGIJI Allahnku.
32 “ ‘Ku miƙe tsaye a gaban tsofaffi, ku nuna bangirma ga waɗanda suka tsufa, ku kuma girmama Allahnku. Ni ne UBANGIJI.
33 “ ‘Sa’ad da baƙo yana zama tare da ku a ƙasarku, kada ku wulaƙanta shi. 34 Dole
ku ɗauki baƙon da yake zama tare da ku kamar haifaffe ɗan ƙasa. Ku ƙaunace shi kamar kanku, gama dā ku ma baƙi ne a Masar. Ni ne UBANGIJI Allahnku.
35 “ ‘Kada ku yi amfani da mudun ƙarya sa’ad da kuke awon tsawo, nauyi, ko yawan
abu. 36 Ku yi amfani da ma’auni na gaskiya da mudu na gaskiya, da kuma magwaji na gaskiya. Ni ne UBANGIJI Allahnku, wanda ya fitar da ku daga Masar.
37 “ ‘Ku kiyaye dukan farillaina da kuma dukan dokokina, ku kuma bi su. Ni ne UBANGIJI.’ ”

# 20

*Hukuntai don zunubi*

1 UBANGIJI ya ce wa Musa, 2 “Faɗa wa Isra’ilawa cewa, ‘Duk wani mutumin Isra’ila
ko baƙon da yake zama a cikin Isra’ila da ya miƙa* wani daga cikin ’ya’yansa wa
Molek, dole sa kashe shi. Mutanen ƙasar za su jajjefe shi. 3 Zan yi gāba da wannan
mutum, zan kuma raba shi da mutanensa; gama ta wurin miƙa ’ya’yansa ga Molek,
ya ƙazantar da wuri mai tsarkina, ya kuma ƙazantar da sunana mai tsarki. 4 In
mutanen ƙasar suka kau da idanunsu sa’ad da wannan mutum ya miƙa ’ya’yansa ga
Molek, suka kāsa kashe shi, 5 zan yi gāba da wannan mutum da iyalinsa, zan raba shi da kuma duk waɗanda suka bi shi cikin karuwanci ga Molek daga mutanensu.
6 “ ‘Zan yi gāba da mutumin da ya juyo ga masu duba da bokaye, don yă yi karuwanci ta wurin bin su, zan kuma raba shi daga mutanensa.
7 “ ‘Ku tsarkake kanku, ku kuma zama da tsarki, gama Ni ne UBANGIJI Allahnku.
8 Ku kiyaye farillaina, ku kuma bi su. Ni ne UBANGIJI, wanda ya mai da ku masu tsarki.†
9 “ ‘In wani ya zagi mahaifinsa ko mahaifiyarsa, dole a kashe shi. Domin ya zagi mahaifinsa ko mahaifiyarsa, alhakin jininsa zai zauna a kansa.
10 “ ‘In mutum ya yi zina da matar wani, da matar maƙwabcinsa, dole a kashe su biyu da suka yi zinan.
11 “ ‘In mutum ya kwana da matar mahaifinsa, ya ƙasƙantar da mahaifinsa. Dole a kashe shi da macen, alhakin jininsu zai zauna a kansu.
12 “ ‘In mutum ya kwana da matar ɗansa, dole a kashe su biyun. Abin da suka yi haram ne; alhakin jininsu zai zauna a kansu.
13 “ ‘In mutum ya kwana da mutum kamar yadda ake kwana da mace, su biyun sun yi abin ƙyama. Dole a kashe su, alhakin jininsu zai zauna a kansu.
14 “ ‘In mutum ya auri ’ya da mahaifiyarta, mugun abu ne. Da shi da su, dole a ƙone su da wuta, saboda kada mugun abu yă kasance a cikinku.

---

* **20:2** Ko kuwa miƙa hadaya; haka ma a ayoyi 3 da 4. † **20:8** Ko kuwa wanda ya tsarkake ku; Ko kuwa wanda ya keɓe masu tsarki

15 " 'In mutum ya yi jima'i da dabba, dole a kashe shi, dole kuma ku kashe dabbar.
16 " 'In mace ta kusaci dabba don tă yi jima'i da ita, ku kashe macen da dabbar.
Dole a kashe su; alhakin jininsu zai zauna a kansu.
17 " 'In mutum ya auri 'yar'uwarsa, ko 'yar mahaifinsa, ko kuwa ta mahaifiyarsa,
suka kuma yi jima'i, abin kunya ne. Dole a raba su a idanun mutanensu. Ya
ƙasƙantar da 'yar'uwarsa kuma za a nemi hakki daga gare shi.
18 " 'In mutum ya kwana da mace a lokacin al'adarta, duka biyunsu za a kore su
daga cikin jama'arsu, gama sun karya ƙa'idodi a kan rashi tsarki.
19 " 'Kada ka yi jima'i da 'yar'uwar mahaifiyarka, ko ta mahaifinka, gama wannan
zai ƙasƙantar da dangi na kurkusa, dukanku za ku ɗauki laifin.
20 " 'In mutum ya kwana da bābarsa, ya ƙasƙantar da kawunsa ke nan. Hakkin
zai kasance a kansu, za su mutu babu 'ya'ya.
21 " 'In mutum ya auri matar ɗan'uwansa, aikin rashin tsabta ne, ya ƙasƙantar da
ɗan'uwansa ke nan. Za su mutu babu 'ya'ya.
22 " 'Ku kiyaye dukan farillaina da dokokina duka, don kada ƙasar da nake kai
ku ta amayar da ku. 23 Kada ku yi zama bisa ga al'adun al'umman da zan kora a
gabanku. Domin sun aikata dukan waɗannan abubuwa, na yi ƙyamarsu. 24 Amma
na faɗa muku, "Za ku mallaki ƙasarsu, zan ba ku ita gādo, ƙasa mai zub da madara
da zuma." Ni ne UBANGIJI Allahnku, wanda ya keɓe ku daga al'ummai.
25 " 'Saboda haka sai ku bambanta tsakanin dabbobi masu tsarki da marasa tsarki,
da kuma tsakanin tsuntsaye masu tsarki da marasa tsarki. Kada ku ƙazantar da
kanku ta wurin wata dabba, ko tsuntsu, ko wani abin da yake rarrafe a ƙasa,
waɗanda na keɓe a matsayi marasa tsarki a gare ku. 26 Ku zama tsarkakakke gare
ni, gama Ni UBANGIJI, mai tsarki ne, na kuma keɓe ku daga al'ummai don ku zama
nawa.
27 " 'Namiji, ko ta macen da yake mai duba, ko maita a cikinku dole a kashe. Za ku
jajjefe su da duwatsu; alhakin jininsu zai zauna a kansu.' "

# 21

*Dokoki domin firistoci*

1 UBANGIJI ya ce wa Musa, "Yi magana da firistoci, 'ya'yan Haruna maza, ka ce
musu, 'Kada firist yă ƙazantar da kansa saboda wani cikin mutanensa da suka mutu,
2 sai dai na danginsa na kusa, kamar mahaifiyarsa ko mahaifinsa, ɗansa ko 'yarsa,
ɗan'uwansa, 3 ko 'yar'uwarsa da ba tă riga ta yi aure ba, wadda take dogara gare shi,
da yake ba ta da miji, saboda ita zai iya ƙazantar da kansa. 4 Kada yă ƙazantar da
kansa saboda mutanen da suke da dangantakar da shi ta wurin aure, ta yin haka zai
ƙazantar da kansa.
5 " 'Kada firistoci su aske kansu ƙwal ko su kwakkwafe gemunsu, ko su tsattsage
jikunansu. 6 Dole su kasance masu tsarki ga Allahnsu, kada kuma su ɓata sunan
Allahnsu. Domin sukan miƙa hadayun da aka kawo wa UBANGIJI da wuta, abincin
Allahnsu, saboda haka sai su kasance da tsarki.
7 " 'Ba za su auri matan da karuwanci ya ɓata su, ko waɗanda mazansu suka sake
su ba, gama firistoci masu tsarki ne ga Allahnsu. 8 An ɗauke su da tsarki, domin suna
miƙa abincin Allahnku. An ɗauka su masu tsarki gama Ni UBANGIJI, mai tsarki ne, Ni
wanda ya mai da ku masu tsarki.
9 " 'In 'yar firist ta ɓata kanta ta wurin zama karuwa, ta kunyatar da mahaifinta ke
nan; dole a ƙone ta da wuta.
10 " 'Babban firist, wanda yake ɗaya cikin 'yan'uwansa wanda aka shafe da mai a
kansa, wanda kuma aka naɗa don yă sa rigunan firistoci, kada yă bar gashin kansa
buzu-buzu, ko ya kyakketa rigunansa. 11 Ba zai shiga inda akwai gawa ba. Kada yă

ƙazantar da kansa, ko ma ta mahaifinsa ce ko ta mahaifiyarsa. 12 An keɓe shi domina,
kada yă ƙazantar da kansa, kada kuwa yă ɓata Tentin Sujada ta wurin shiga gidan
da gawa take, ko ta mahaifinsa, ko ta mahaifiyarsa ce. Ni ne Ubangiji.

13 " 'Dole macen da zai aura ta kasance budurwa. 14 Ba zai auri matan da mijinta
ya mutu, ko macen da mijinta ya rabu da ita, ko macen da ta ɓata kanta ta wurin
karuwanci ba, sai dai yă auri budurwa daga cikin mutanensa, 15 don kada yă ƙazantar
da 'ya'yansa a cikin mutanensa. Ni ne Ubangiji, wanda ya mai da shi mai tsarki.' "

16 Ubangiji ya ce wa Musa, 17 "Faɗa wa Haruna cewa, 'Don tsararraki masu zuwa,
kada ko ɗaya daga cikin zuriyarka, da yake da lahani yă zo kusa domin yă miƙa
hadaya ta ci gare ni. 18 Duk mai lahani, ko makaho, ko gurgu, ko mai naƙasa, ko
mai wani lahani a jiki; 19 ko mai karyayyen ƙafa, ko mai karyayyen hannu, 20 ko mai
ƙusumbi, ko wada, ko wanda yake da lahani a ido, ko mai cuta mai sa ƙaiƙayi, ko
mai kirci, ko wanda aka daƙe, ba zai yi kusa domin yă miƙa hadaya ba. 21 Ba zuriyar
Haruna firist, mai lahanin da zai zo kusa don yă miƙa hadayun da aka yi ga Ubangiji
da wuta. Da yake yana da lahani, ba zai zo kusa don yă miƙa abincin Allahnsa ba.
22 Zai iya cin abinci mafi tsarki na Allahnsa, haka ma abinci mai tsarki; 23 duk da
haka saboda lahaninsa, ba zai yi kusa da labule, ko yă yi kusa da bagade don kada yă
ƙazantar da wuri mai tsarkina. Ni ne Ubangiji wanda yake mai da su masu tsarki.' "

24 Sai Musa ya faɗa wannan wa Haruna da 'ya'yansa maza da kuma dukan
Isra'ilawa.

# 22

1 Ubangiji ya ce wa Musa, 2 "Faɗa wa Haruna da 'ya'yansa maza, su lura da
tsarkakakkun abubuwan da Isra'ilawa suka keɓe gare ni da bangirma, saboda ba
za su ƙazantar da sunana mai tsarki ba. Ni ne Ubangiji.

3 "Faɗa musu cewa, 'Don tsararraki masu zuwa, in wani zuriyarku ya ƙazantu, duk
da haka ya kusaci tsarkakakku hadayun da Isra'ilawa suka keɓe ga Ubangiji, dole a
raba wannan mutum daga gabana. Ni ne Ubangiji.

4 " 'In zuriyar Haruna yana da kuturu, ko mai ɗiga, ba zai ci daga cikin
tsarkakakkun abubuwa ba, sai lokacin da ya tsarkaka. Duk wanda ya taɓa wani
abu marar tsarki na mamaci, ko wanda maniyyinsa yake ɗiga, 5 da duk kuma wanda
ya taɓa wani abu mai rarrafe wanda yake ƙazantarwa, ko kuwa wani mutum mai
ƙazanta, 6 duk mutumin da ya taɓa kowane irin abu haka, zai ƙazantu har yamma,
ba kuwa zai ci daga cikin tsarkakakkun abubuwan nan ba, sai ya yi wanka tukuna.
7 Sa'ad da rana ta fāɗi, zai zama tsarkakakke, bayan wannan kuwa zai iya cin
tsarkakakkun hadayu, gama abincinsa ne. 8 Kada yă ci wani abin da ya mutu mushe,
ko wanda namun jeji suka yayyaga, don kada yă ƙazantar da kansa. Ni ne Ubangiji.

9 " 'Firistoci za su kiyaye umarnaina don kada su yi laifi su mutu saboda sun rena
su. Ni ne Ubangiji, wanda ya mai da su masu tsarki.

10 " 'Duk wanda ba daga cikin iyalin firistoci ba, ko da yake yana zama tare da
su, ko kuwa an ɗauke shi yana yin musu aiki, ba zai ci daga cikin tsarkakakkun
hadayun ba. 11 Amma in firist ya sayi bawa da kuɗi, ko kuwa in an haifi bawan a
gidansa, wannan bawan zai iya cin tsattsarkan abincin. 12 In 'yar firist ta auri wani
da ba firist ba, ba za tă ci wani tsarkakakkun sadaka ba. 13 Amma idan 'yar firist ta
zama gwauruwa ko sakakkiya, ba ta da 'ya'ya, ta kuwa dawo don tă zauna a gidan
mahaifinta kamar matashiya, za tă iya cin abincin.

14 " 'In wani ya ci tsarkakakken abinci cikin kuskure, dole yă maido wa firist
hadayar, yă kuma ƙara kashi ɗaya bisa biyar na tamanin abin. 15 Firist ɗin ba zai
ƙasƙantar da tsarkakakkun hadayun da Isra'ilawa suka kawo ga Ubangiji 16 ta wurin

barinsu su ci tsarkakakkun hadayu, ta yin haka su jawo wa kansu laifin da zai bukaci
biya ba. Ni ne UBANGIJI, wanda ya mai da ku masu tsarki.’ ”

### *Hadayun da ba a yarda da su ba*

17 UBANGIJI ya ce wa Musa, 18 “Yi wa Haruna da ’ya’yansa maza da kuma dukan
Isra’ilawa magana ka ce musu, ‘In waninku, ko mutumin Isra’ila, ko baƙon da yake
zama a Isra’ila, ya kawo kyauta don hadaya ta ƙonawa ga UBANGIJI, ko don yă cika
alkawari, ko kuwa a matsayin hadaya ta yardar rai, 19 dole ku miƙa dabba namiji
marar lahani, daga shanu, tumaki, ko awaki, domin yă zama yardajje a madadinku.
20 Kada ku kawo wani abu mai lahani, domin ba zai zama yardajje ba a madadinku.
21 Sa’ad da wani ya kawo hadaya ta salama daga garken shanu, ko na tumaki, ga
UBANGIJI don yă cika wani alkawari na musamman, ko hadaya ta yardar rai, dole
yă zama marar lahani, ko tabo, don yă zama yardajje. 22 Kada ku miƙa wa UBANGIJI
dabbobi makafi, ko naƙasassu, ko masu gundumi, ko masu ɗiga, ko masu susa, ko
masu kirci. Kada ku sa wani daga cikin waɗannan a bisa bagade a matsayin hadaya,
gama hadaya ce da aka ƙone da wuta ga UBANGIJI. 23 Za ku iya miƙa hadaya ta yardar
rai da maraƙi, ko tunkiya mai naƙasa, ko marar cikakken lafiya, amma ba za tă zama
yardajje don cika alkawarin da aka yi ba. 24 Ba za ku miƙa wa UBANGIJI dabbar da
lunsayinta yake da ƙujewa, ko dandaƙewa, ko yagewa, ko yankewa ba. 25 Ba za ku
kuma karɓi irin waɗannan dabbobi daga hannun baƙi ku miƙa su a matsayin abinci
ga Allahnku ba. Ba za su zama yardajje a madadinku ba, domin sun naƙasa, suna
kuma da lahani.’ ”
26 UBANGIJI ya ce wa Musa, 27 “Sa’ad da aka haifi ɗan maraƙi, tunkiya, ko akuya,
sai yă kasance da mahaifiyarsa kwana bakwai. Daga rana ta takwas zuwa gaba, zai
zama yardajje hadaya, hadaya ce da aka ƙone da wuta ga UBANGIJI. 28 Kada a yanka
saniya, ko tunkiya da ɗanta rana ɗaya.
29 “Sa’ad da kuka miƙa hadaya ta godiya ga UBANGIJI, ku miƙa ta a yadda za tă
zama yardajje a madadinku. 30 Dole a ci hadayar a ranar; kada a bar saura sai da
safe. Ni ne UBANGIJI.
31 “Ku kiyaye dokokina, ku kuma bi su. Ni ne UBANGIJI. 32 Kada ku ƙasƙantar da
sunana mai tsarki. Dole Isra’ilawa su gane Ni mai tsarki ne. Ni ne UBANGIJI, wanda
ya keɓe ku a matsayin tsarkaka 33 da kuma wanda ya fitar da ku daga Masar don in
zama Allahnku. Ni ne UBANGIJI.”

## 23

1 UBANGIJI ya ce wa Musa, 2 “Yi magana da Isra’ilawa, ka ce musu, ‘Ga ƙayyadaddun
bukukkuwa, ƙayyadaddun bukukkuwan UBANGIJI, da za ku sanar wa mutane su riƙa
kiyayewa, su zama lokutan tarurruka masu tsarki.

### *Asabbaci*

3 “ ‘Akwai kwanaki shida da za ku iya yin aiki, amma rana ta bakwai, Asabbaci ne
na hutu, rana mai tsarki ga jama’a. Kada ku yi wani aiki a ko’ina kuke da zama,
Asabbaci ne ga UBANGIJI.

### *Bikin Ketarewa da Burodi Marar Yisti*
*(Kidaya 28.16-25)*

4 “ ‘Waɗannan su ne bukukkuwan da UBANGIJI ya kafa da tsarkakakkun taron
jama’a za su yi a ƙayyadaddun lokuta. 5 Bikin Ketarewar UBANGIJI, zai fara da
yamma a ranar goma sha huɗu na wata na fari. 6 A rana ta goma sha biyar na
wannan wata, za a fara Bikin Burodi Marar Yisti na UBANGIJI. Za ku yi kwana bakwai
kuna cin burodi marar yisti. 7 A rana ta fari, ku yi taro mai tsarki, ba kuwa za ku yi

aiki na kullum ba. 8 Kwana bakwai za ku miƙa hadaya ga Ubangiji da wuta. A rana
ta bakwai ɗin ku yi taro mai tsarki, ba za ku kuwa yi aiki na kullum ba.' "

### *'Ya'yan fari na itatuwa*

9 Ubangiji ya ce wa Musa, 10 "Yi magana da Isra'ilawa, ka ce musu, 'Sa'ad da kuka
shiga ƙasar da zan ba ku, kuka kuma girbe amfanin gonarta, sai ku kawo wa firist
damin hatsi na farko da kuka girbe. 11 Zai kaɗa damin a gaban Ubangiji domin yǎ
zama yardajje a madadinku; firist ɗin zai kaɗa shi a kashegarin Asabbaci. 12 A ranar
da kuka kaɗa damin, dole ku miƙa hadaya ta ƙonawa na ɗan rago bana ɗaya, marar
lahani ga Ubangiji, 13 tare da hadaya ta gari mai laushi, humushi biyu haɗe da mai,
wato, hadaya ce da aka ƙone da wuta ga Ubangiji, mai daɗin ƙanshi, da kuma abin
sha kwalaba ɗaya na ruwan inabi. 14 Ba za ku ci wani burodi, ko gasasshen hatsi, ko
sabon hatsi ba, sai ran nan da kuka kawo wannan hadaya ga Allahnku. Wannan za
tǎ zama dawwammamiyar farilla wa tsararraki masu zuwa, a duk inda kuke zama.

### *Bikin Makoni*
### *(Kidaya 28.26-31)*

15 " 'Daga kashegarin Asabbaci, ranar da kuka kawo dami don hadaya ta kaɗawa,
ku ƙirga cikakku makoni bakwai. 16 Ku ƙirga kwana hamsin har zuwa kashegarin
Asabbaci na bakwai, sa'an nan ku miƙa hadaya ta sabon hatsi ga Ubangiji. 17 Daga
ko'ina kuke da zama, ku kawo dunƙule biyu na humushin gari mai laushi da aka
tuya da yisti, a matsayin hadaya ta kaɗawa ta 'ya'yan fari na itatuwa ga Ubangiji.
18 Tare da wannan, ku miƙa 'yan raguna bakwai, kowanne bana ɗaya-ɗaya marar
lahani, bijimi da kuma raguna biyu. Za su zama hadaya ta ƙonawa ga Ubangiji, tare
da hadayunsu na hatsi, da hadayunsu na sha, hadaya da aka yi da wuta, mai daɗin
ƙanshi ga Ubangiji. 19 Sa'an nan ku miƙa bunsuru ɗaya na hadaya don zunubi, da
'yan raguna biyu, kowanne bana ɗaya-ɗaya, don hadaya ta salama. 20 Firist zai kaɗa
'yan raguna biyun a gaban Ubangiji, a matsayin hadaya ta kaɗawa, tare da burodin
sababbin 'ya'yan fari na itatuwan. Tsarkaken hadaya ce ga Ubangiji ga firist. 21 A
wannan rana za ku yi taro mai tsarki, ba kuwa za ku yi aiki na kullum ba. Wannan za
tǎ zama dawwammamiyar farilla wa tsararraki masu zuwa, a ko'ina kuke da zama.
22 " 'Sa'ad da kuka yi girbin gonarku, kada ku girbe har ƙarshen gefen gonar, ko
ku yi kalar girbinku. Ku bar su wa matalauta da baƙi. Ni ne Ubangiji Allahnku.' "

### *Bikin busar ƙahoni*
### *(Kidaya 29.1-6)*

23 Ubangiji ya ce wa Musa, 24 "Faɗa wa Isra'ilawa cewa, 'A ranar farko ga wata na
bakwai, za tǎ zama ranar hutu, rana ce ta tuni da yin taro mai tsarki na sujada da za
a fara busar ƙaho. 25 Kada ku yi aiki na kullum, amma ku miƙa hadaya ta ƙonawa
ga Ubangiji.' "

### *Ranar kafara*
### *(Kidaya 29.7-11)*

26 Ubangiji ya ce wa Musa, 27 "Rana ta goma ta wata bakwai, za tǎ zama Ranar
Kafara. Sai ku yi taro mai tsarki don ku yi mūsun kanku ku kuma miƙa hadayar
da aka yi da wuta ga Ubangiji. 28 Kada ku yi aiki a ranar, gama Ranar Kafara ce,
sa'ad da za a yi kafara saboda ku a gaban Ubangiji Allahnku. 29 Duk wanda bai yi
mūsun kansa a wannan rana ba, dole a raba shi daga mutanensa. 30 Zan hallaka duk
wani da ya yi aiki a wannan rana daga mutanensa. 31 Sam ba za ku yi wani aiki ba.
Wannan za tǎ zama dawwammamiyar farilla ce, wa tsararraki masu zuwa, a ko'ina
kuke da zama. 32 Asabbaci ne na hutu dominku, kuma dole ku yi mūsun kanku. Daga
yamman rana ta tara ga wata, har zuwa yamma na biye, za ku kiyaye Asabbacinku."

*Bikin tabanakul*
*(Kidaya 29.12-40)*
33 UBANGIJI ya ce wa Musa, 34 “Faɗa wa Isra'ilawa cewa, 'A ranar goma sha biyar
ga wata na bakwai, za a fara Bikin Tabanakul na UBANGIJI, zai kuma ɗauki kwana
bakwai. 35 A ranar farko za tă zama ta taro mai tsarki, kada ku yi aiki na kullum.
36 Kwana bakwai za ku miƙa hadayun da aka yi da wuta ga UBANGIJI, a rana ta takwas,
ku yi taro mai tsarki, ku kuma miƙa hadayar da aka yi da wuta ga UBANGIJI. Wannan
ranar rufewar taro ce; kada ku yi aiki na kullum.
37 (“ 'Waɗannan su ne bukukkuwan da UBANGIJI ya kafa, waɗanda za ku yi a
matsayin tsarkakakkun taro, don kawo hadayun da aka yi da wuta ga UBANGIJI,
hadayu na ƙonawa da hadayu na hatsi, sadaka da kuma hadayu na sha, da ake
bukata kowace rana. 38 Waɗannan hadayu, ƙari ne a kan waɗannan na Asabbatan
UBANGIJI, haɗe kuma da kyautanku, da kome da kuka yi alkawari, da kuma hadayu
yardar ran da za ku ba wa UBANGIJI.)
39 “ 'Saboda haka, farawa daga ranar goma sha biyar ga watan bakwai, bayan kun
tara hatsin gona, ku yi bikin UBANGIJI kwana bakwai; rana ta fari, rana hutu ce, rana
ta takwas kuma rana hutu ce. 40 A rana ta fari, za ku ɗebi zaɓaɓɓun 'ya'yan itatuwa
daga itatuwa, da rassan dabino, rassa masu ganye, da kuma ganyayen itacen wardi
na rafi, ku yi farin ciki a gaban UBANGIJI Allahnku, kwana bakwai. 41 Za ku kiyaye
bikin nan har kwana bakwai a kowace shekara ga UBANGIJI. Wannan za tă zama
dawwammamiyar farilla wa tsarraraki masu zuwa, ku kiyaye ta a wata na bakwai.
42 Ku zauna a bukkoki kwana bakwai. Dukan 'yan ƙasa haifaffun Isra'ilawa, za su
zauna a bukkoki 43 don zuriyarku tă san cewa na sa Isra'ilawa suka zauna a bukkoki
sa'ad da na fitar da su daga Masar. Ni ne UBANGIJI Allahnku.' ”
44 Saboda haka Musa ya sanar wa Isra'ilawa ƙayyadaddun bukukkuwan UBANGIJI.

# 24

*Mai da burodi, shiryayye a gaban UBANGIJI*
*(Fitowa 27.20,21)*
1 UBANGIJI ya ce wa Musa, 2 “Ka umarci Isra'ilawa su kawo tsabtataccen mai na
zaitun da aka matse, don ƙuna fitilun yadda harshen wutar ba zai taɓa mutuwa
ba. 3 Za a ajiye su waje da labulen Wuri Mafi Tsarki a Tentin Sujada, Haruna zai
riƙa kula da fitilun a gaban UBANGIJI, daga yamma zuwa safiya. Wannan za tă zama
dawwammamiyar farilla wa tsararraki masu zuwa. 4 Dole a ci gaba da shirya fitilu
a kan wurin ajiye fitila na zinariya, a gaban UBANGIJI.
5 “Ɗauki gari mai laushi a gasa dunƙulen burodi goma sha biyu, a yi amfani da
humushi biyu na garwan gari don kowace burodi. 6 A shirya su jeri biyu, guda shida
a kowane jeri a kan teburin da aka yi da zinariya zalla, a gaban UBANGIJI. 7 Za a zuba
turare a kowane layin dunƙulen burodin don yă kasance abin tunawa a bisa burodin.
Turaren zai ƙone a madadin burodin don yă zama kamar hadayar da aka miƙa da
wuta ga UBANGIJI. 8 Za a shirya wannan gurasa a gaban UBANGIJI kowane Asabbaci, a
madadin Isra'ilawa a matsayin madawwamin alkawari. 9 Wannan burodin zai zama
na Haruna da 'ya'yansa maza, waɗanda za su ci a tsattsarkan wuri, gama sashe ne
mafi tsarki na rabonsu na kullum na hadayar da aka yi da wuta ga UBANGIJI.”

*A Jajjefi mai saɓo da duwatsu*
10 To, ɗan wata mutuniyar Isra'ila wanda mahaifinsa mutumin Masar ne, ya je
cikin Isra'ilawa, sai faɗa ta tashi tsakaninsa da wani mutumin Isra'ila a cikin sansani.
11 Ɗan mutuniyar Isra'ila ya saɓi Sunan UBANGIJI, ya kuma la'ana shi, saboda haka
aka kawo shi wa Musa. (Sunan mahaifiyarsa Shelomit ne, 'yar Dibri na kabilar Dan.)

[12] Suka sa shi a gidan tsaro sai lokacin da nufin UBANGIJI ya nuna musu abin da za
su yi da shi.
[13] Sai UBANGIJI ya ce wa Musa, [14] "Ka kai mai saɓon nan waje da sansani. Duk
waɗanda suka ji maganar da mai saɓon nan ya yi su ɗibiya hannuwansu a kansa,
taron jama'a kuwa gaba ɗaya su jajjefe shi da duwatsu. [15] Faɗa wa Isra'ilawa cewa,
'Duk wanda ya zagi Allahnsa, alhakin zai rataya a wuyansa, [16] duk wanda ya saɓi
sunan UBANGIJI, dole a kashe shi. Dole jama'a gaba ɗaya su jajjefe shi da duwatsu.
Ko baƙo, ko haifaffen ɗan ƙasa, sa'ad da ya saɓi Sunan UBANGIJI, dole a kashe shi.
[17] " 'Duk wanda ya kashe mutum, dole a kashe shi. [18] Duk wanda ya kashe dabbar
wani, dole yă biya, rai domin rai. [19] Duk wanda ya yi wa maƙwabcinsa rauni, sai a
yi masa abin da ya yi; [20] karaya don karaya, ido don ido, haƙori don haƙori. Kamar
yadda ya yi wa wani rauni, shi ma a yi masa. [21] Duk wanda ya kashe dabba, dole yă
biya, amma duk wanda ya kashe mutum, dole a kashe shi. [22] Za ku kasance da doka
iri ɗaya wa baƙo da kuma wa haifaffen ɗan ƙasa. Ni ne UBANGIJI Allahnku.' "
[23] Sai Musa ya yi wa Isra'ilawa magana, suka kuwa kai mai saɓon waje da sansani,
suka jajjefi shi da duwatsu. Isra'ilawa suka yi yadda UBANGIJI ya umarci Musa.

# 25

*Shekara ta Asabbaci*
*(Maimaitawar Shari'a 15.1-11)*

[1] UBANGIJI ya yi magana da Musa a kan Dutsen Sinai ya ce, [2] "Yi wa Isra'ilawa
magana, ka ce musu, 'Sa'ad da kuka shiga ƙasar da zan ba ku, dole ƙasar kanta ta
kiyaye Asabbaci ga UBANGIJI. [3] Shekara shida, za ku yi shuki, shekara shida kuma za
ku aske gonakin inabinku, ku kuma tattara hatsinsu. [4] Amma a shekara ta bakwai,
ƙasar za tă sami hutun Asabbaci, Asabbaci ga UBANGIJI. Kada ku yi shuki a gonakinku,
ko kuwa ku aske gonakinku na inabi. [5] Kada ku girbe abin da ya yi girma ba tare
da ku kuka shuka ba, ko ku girbe inabin da ba ku aske ba. Kasar za tă kasance da
shekarar hutu. [6] Duk abin da gonar ta ba da amfani a shekara ta Asabbaci, zai zama
abinci gare ku, wa kanku, bayinku maza da mata, da ma'aikatan da kuka ɗauka aiki,
da kuma waɗanda ba zama ɗinɗinɗin suke yi tare da ku ba, [7] haka ma zai zama
abinci domin dabbobinku, da kuma namun jeji a ƙasarku. Duk abin da ƙasar ta
bayar za a ci.

*Murnar cika shekarar hamsin*

[8] " 'Ku ƙirga asabbatai bakwai na shekaru bakwai, sau bakwai. Gama asabbatai
bakwai na shekaru bakwai za su yi daidai da shekaru arba'in da tara. [9] Sa'an nan a
busa ƙaho a ko'ina, a rana ta goma ga wata na bakwai; a Ranar Kafara, a busa ƙaho
a dukan ƙasarku. [10] Ku keɓe shekara ta hamsin ku kuma yi shelar 'yanci a dukan
ƙasar ga mazaunanta. Za tă zama shekarar murna gare ku; kowannenku zai koma
ga mallakar iyalinsa, kuma kowa ga danginsa. [11] Shekara ta hamsin za tă zama ta
murna a gare ku; kada ku yi shuki, kada kuma ku yi girbi abin da ya yi girma da
kansa, ko ku girbe inabin da ba ku lura da shi ba. [12] Gama shekara ce ta murna, za tă
kuma zama mai tsarki a gare ku, ku dai ci abin da aka ɗauka kai tsaye daga gonaki.
[13] " 'A wannan Shekara ta Murna, kowa zai koma ga mallakarsa.
[14] " 'In ka sayar da gona wa wani daga mutanen ƙasarka, ko ka saya wata gona
daga gare shi, kada ku cuci juna. [15] Sa'ad da mutum ya sayi fili daga abokin zamansa,
kuɗin zai kasance bisa ga yawan shekara hamsin ta murna da suka wuce, da kuma
bisa ga yawan shekarun noma da suka rage kafin wata shekara hamsin ta murna.
[16] Idan shekarun suna da yawa, sai ku kara kuɗin filin, idan kuma shekarun ba su

da yawa, sai ku rage kuɗin filin, gama ainihin abin da ake sayar maka shi ne yawan
hatsin. [17] Kada ku cuci juna, amma ku ji tsoron Allahnku. Ni ne UBANGIJI Allahnku.
[18] “ ‘Ku bi farillaina, ku kuma yi hankali ga kiyaye dokokina, za ku kuwa zauna
lafiya a ƙasar. [19] Sa’an nan ƙasar za tă ba da amfaninta, za ku kuwa ci ku ƙoshi, ku
kuma zauna lafiya. [20] Mai yiwuwa ku ce, “Me za mu ci a shekara ta bakwai in ba
mu yi shuki ko girbin hatsinmu ba?” [21] Zan aika muku da irin albarka a shekara ta
shida har da ƙasar za tă ba da amfani isashe na shekara uku. [22] Yayinda kuke shuki
a shekara ta takwas, za ku kasance da raguwa hatsi na shekarar da ta wuce, za ku
kuma ci gaba da ci daga gare shi har girbin shekara ta tara yă shigo.
[23] “ ‘Kada a sayar da gona ɗinɗinɗin, gama ƙasar tawa ce, ku kuwa baƙi ne kawai,
kuma ’yan haya nawa. [24] Ko’ina a ƙasar da kuke da mallaka, dole ku tanadar da
dama fansar ƙasar.
[25] “ ‘In ɗaya daga cikin mutanen ƙasarku ya talauta, ya kuma sayar da mallakarsa,
sai danginsa na kusa yă je yă fanshi abin da mutumin ƙasarsa ya sayar. [26] In mutumin
ba shi da wanda zai fansa masa ita, shi kansa kuwa ya wadace, ya kuma sami isashen
halin fansarta, [27] sai yă lasafta yawan shekarun da aka yi tun da an sayar da filin.
Kuɗin filin zai dangana ga yawan shekarun da suka rage kafin shekara hamsin ta
murna da za tă zo; sa’an nan zai iya koma ga mallakarsa. [28] Amma in bai sami halin
sāke biyansa ba, abin nan da ya sayar zai ci gaba da zama mallakar mai sayan, sai
Shekara ta Murna. Za a maido masa da ita a Shekara ta Murna, sa’an nan zai iya
koma ga mallakarsa.
[29] “ ‘In mutum ya sayar da gida a birni mai katanga, yana da izini yă fanshe shi a
ƙarshen shekara guda, bayan ya sayar da shi. [30] In ba a fanshe shi a ƙarshen shekara
ba, gidan da yake a birni mai katanga, zai zama mallakar na ɗinɗinɗin na mai sayan
da kuma zuriyarsa. Ba za a mai da shi a Shekara ta Murna ba. [31] Amma za a ɗauki
gidaje a ƙauyuka marasa katanga kewaye da su daidai da gonaki. Za a iya fanshe su,
a kuma mayar da su a Shekara ta Murna.
[32] “ ‘Kullum, Lawiyawa suna da izini su fanshi gidajensu a biranen Lawiyawa
waɗanda suka mallaka. [33] Saboda haka ana iya fansa mallakar Lawiyawa, wato,
gidan da aka sayar a duk birnin da yake nasu, za a kuma mayar a Shekara ta Murna,
gama gidaje a biranen Lawiyawa, mallakar Isra’ilawa ne. [34] Amma kada a sayar da
filayen kiwo na waɗannan birane; mallakarsu ce, ta ɗinɗinɗin.
[35] “ ‘In ɗaya daga ciki mutanen ƙasarku ya talauta, ba ya kuma iya tallafa wa kansa
a cikinku, sai ku taimake shi kamar yadda za ku yi da baƙo a cikinku. [36] Kada ku
karɓi riba ta kowace iri daga gare shi, amma ku ji tsoron Allahnku, saboda mutumin
ƙasarku yă ci gaba da zama a cikinku. [37] Kada ku ba shi rancen kuɗi da ruwa, ko ku
sayar masa abinci don samun riba. [38] Ni ne UBANGIJI Allahnku, wanda ya fitar da ku
daga Masar, don in ba ku ƙasar Kan’ana in kuma zama Allahnku.
[39] “ ‘In ɗaya daga cikin mutanen ƙasarku ya talauta a cikinku, ya kuma sayar da
kansa gare ku, kada ku sa yă yi kamar bawa. [40] Amma a ɗauke shi a matsayin
ma’aikacin da aka ɗauka aiki, ko mazaunan da ba na ɗinɗinɗin ba a cikinku, sai yă
yi muku aiki sai Shekara ta Murna. [41] Sa’an nan a sake shi da ’ya’yansa, yă kuma
koma ga danginsa da mallakar kakanninsa. [42] Gama Isra’ilawa bayina ne, waɗanda
na saya daga Masar, kada a sayar da su a matsayin bayi. [43] Kada ku gwada musu
azaba, amma ku ji tsoron Allahnku.
[44] “ ‘Bayinku maza da mata, za su zo daga al’ummai da suke kewaye da ku, daga
gare su za ku iya saya bayi. [45] Za ku iya saya waɗansu mutanen da ba sa zama
ɗinɗinɗin a cikinku, da kuma membobin danginsu da aka haifa a ƙasarku. [46] Za ku
iya ba da su ga ’ya’yanku a matsayin kayan gādo, za ku kuma iya mai da su bayi
dukan rayuwarsu, amma kada ku yi mulki a bisa ’yan’uwanku Isra’ilawa da tsanani.

47 “ ‘In baƙo, ko wani da yake zama ba na ɗinɗinɗin ba a cikinku, ya wadace, ɗaya
daga cikin mutanen ƙasarku kuwa ya talauta, ya kuma sayar da kansa ga baƙon
da yake zama a cikinku, ko memba na dangin baƙon, 48 yana da izini samun fansa,
bayan ya sayar da kansa. Ɗaya daga cikin danginsa zai iya fansarsa. 49 Kawu ko
yaron ɗan’uwan mahaifin wannan mutum, ko kuwa wani dangi a cikin zuriyarsa,
zai iya fanshe shi. Ko kuma in ya azurta, zai iya fansar kansa. 50 Da shi da mai
sayansa, za su ƙirga lokaci daga shekarar da ya sayar da kansa har zuwa Shekara ta
Murna. Farashin sakinsa zai dangana a kuɗin da ake biyan ma’aikacin da aka ɗauka
aiki, na yawan shekarun ne. 51 In shekaru sun ragu, dole yă biya don fansarsa da
kuɗi mai yawa fiye da wanda aka saye shi. 52 In shekarun sun rage kaɗan ne kafin
Shekara ta Murna, sai yă yi lissafin wannan, yă kuma biya fansarsa daidai wa daida.
53 Sai a yi da shi kamar ma’aikacin da aka ɗauka aiki, daga shekara zuwa shekara;
dole ku tabbata mai shi bai mallake shi da tsanani ba.
54 “ ‘Ko ma ba a fanshe shi a ɗaya daga cikin waɗannan hanyoyi ba, sai a sake shi
da ’ya’yansa a Shekara ta Murna, 55 gama Isra’ilawa nawa ne a matsayin bayi. Su
bayina ne waɗanda na saya daga Masar. Ni ne UBANGIJI Allahnku.

# 26

### *Lada don biyayya*

1 “ ‘Kada ku yi gumaka, ko ku kafa siffa, ko al’amudi wa kanku, kada kuma ku sa
sassaƙaƙƙun duwatsu a ƙasarku don ku rusuna musu. Ni ne UBANGIJI Allahnku.
2 “ ‘Ku kiyaye Asabbataina, ku kuma ba wa wuri mai tsarkina girma. Ni ne UBANGIJI.
3 “ ‘In kuka kiyaye farillaina, kuka yi biyayya da umarnaina, 4 zan aika da ruwan
sama a lokacinsa, ƙasa kuma za tă ba da hatsi, itatuwa kuma za su haihu ’ya’yansu.
5 Masussukanku za su ci gaba har lokacin girbin inabi, girbin inabi kuma zai ci gaba
har lokacin shuki, za ku kuma ci duk abincin da kuke so cikin salama a ƙasarku.
6 “ ‘Zan ba ku salama a ƙasar, za ku kuwa kwanta, kuma babu wani da zai tsorata
ku. Zan kori mugayen namun jeji daga ƙasar, takobi kuma ba zai ratsa cikin ƙasarku
ba. 7 Za ku kori abokan gābanku, za su kuwa fāɗi a kaifin takobi a gabanku.
8 Mutanenku biyar za su kori mutum ɗari, mutanenku ɗari kuma za su kori mutane
dubu goma, abokan gābanku kuma za su fāɗi a kaifin takobi a gabanku.
9 “ ‘Zan dube ku da idon rahama, in kuma sa ku riɓaɓɓanya ku kuma ƙaru, zan
kiyaye alkawarina da ku. 10 Za ku ci gaba da cin girbin bara, har ku fitar da shi don
ku sami wurin saboda sabo. 11 Zan kafa wurin zamana a cikinku, ba zan kuma yi
ƙyamarku ba. 12 Zan yi tafiya a cikinki in kuma zama Allahnku, za ku kuwa zama
mutanena. 13 Ni ne UBANGIJI Allahnku, wanda ya fitar da ku daga Masar don kada ku
ƙara zama bayi ga Masarawa; na karya sandunan wahalarku, na kuma bar ku ku yi
tafiya a sake.

### *Hukunci don rashin biyayya*

14 “ ‘Amma in za ku kasa kunne gare ni, ku kuma aikata dukan waɗannan umarnai,
15 in kuka kuma ƙi farillaina, kuka yi ƙyamar dokokina, kuka kuma kāsa kiyaye
umarnaina, har kuka karya alkawarina, 16 to, zan yi muku wannan. Zan kawo muku
abin bantsoro, cututtuka da zazzaɓin da zai lalatar da idonku, yă kuma sa ranku a
wahala. Za ku shuka iri a banza, domin abokan gābanku ne za su ci. 17 Zan yi gāba
da ku har abokan gābanku su ci ku a yaƙi, su waɗanda suke ƙinku za su yi mulki a
kanku, za ku gudu ba tare da wani yana korinku ba.
18 “ ‘In bayan dukan wannan, ba ku saurare ni ba, zan hukunta ku saboda
zunubanku har sau bakwai. 19 Zan karya ikonku wanda kuke fariya da shi, in hana

ruwan sama, ƙasa kuma tă zama kamar tagulla. [20] Karfinku zai ƙare a banza domin
ƙasarku ba za tă ba da hatsi ba, balle itatuwan ƙasar su ba da ʼyaʼya.

[21] “ ʻIn kuka ci gaba da tayar mini, kuka ƙi ku saurare ni, zan ninka wahalolinku
sau bakwai, yadda ya dace da zunubanku. [22] Zan aika da mugayen namun jeji a
kanku, za su kuwa kashe ʼyaʼyanku, su hallaka shanunku, su rage yawanku, ku zama
kaɗan. Wannan zai sa a rasa mutane a kan hanyoyinku.

[23] “ ʻIn duk da waɗannan abubuwa, ba ku yarda da gyaran da nake yi muku ba,
kuka ci gaba da yin adawa da ni, [24] zan yi adawa da ku, zan kuma aukar muku saboda
zunubanku har sau bakwai. [25] Zan kawo takobi a kanku don in yi ramuwa saboda
karya alkawarin da kuka yi. Saʼad da kuka janye zuwa cikin biranenku, zan aika da
annoba a cikinku, za a kuwa ba da ku ga hannun abokan gāba. [26] Saʼad da na yanke
abincinku, mata goma za su dafa abinci a murhu ɗaya, za su kuma rarraba abincin
a maʼauni. Za ku ci amma ba za ku ƙoshi ba.

[27] “ ʻIn duk da haka kuka ci gaba da ƙin saurare ni, kuka ci gaba da yin adawa da ni,
[28] cikin fushina, sai in yi adawa da ku, in kuma hukunta ku saboda zunubanku har sau
bakwai. [29] Za ku ci naman ʼyaʼyanku maza da na ʼyaʼyanku mata. [30] Zan rurrushe
dukan masujadanku, in yanke bagadanku na turare, in yi tarin gawawwakinku a
kan gumakanku, zan kuma yi ƙyamarku. [31] Zan mai da biranenku kango, in lalace
wuraren tsarkinku, ba zan kuma shaƙi ƙanshi hadayunku ba. [32] Zan mai da ƙasarku
kango har abokan gābanku da suke zama a wurin su yi mamaki. [33] Zan watsar da ku
cikin alʼummai, in kuma ja takobina in kore ku. Kasarku za tă zama kufai, biranenku
kuma su zama kango. [34] Saʼan nan ƙasar za tă ji daɗin hutun shekarun Asabbacinta,
a dukan lokutan da take kango, ku kuwa kuna a ƙasar abokan gābanku, saʼan nan
ƙasar za tă huta ta ji daɗin asabbatanta. [35] A dukan lokutan da take kango, ƙasar za
tă sami hutun da ba tă samu a lokutan asabbatan da kuke zama a cikinta ba.

[36] “ ʻGa waɗanda za su ragu kuwa, zan cika zukatansu da tsoro a ƙasashen abokan
gābansu har motsin ganyen da iska ta hura zai sa su ruga da gudu. Za su yi gudu
kamar suna gudu daga takobi ne, za su kuma fāɗi, ko da yake babu wanda yake
korinsu. [37] Za su yi karo da juna kamar waɗanda suke tsere wa takobi, ko da yake
babu wanda yake korinsu. Ta haka ba za ku iya tsaya a gaban abokan gābanku ba.
[38] Za ku mutu a cikin alʼummai, ƙasar abokan gābanku za tă cinye ku. [39] Sauranku
da suka ragu za su lalace a ƙasashen abokan gābansu saboda zunubansu; da kuma
saboda zunuban kakanninsu.

[40] “ ʻAmma in suka tuba daga zunubansu da zunuban kakanninsu, da cin amanar da
suka yi mini, da kuma adawar da suka yi da ni, [41] waɗanda suka sa na yi adawa da su
har da na aika da su ƙasar abokan gābansu, saʼad da suka ƙasƙantar da zukatansu
marasa kaciya, suka kuma biya hukuncin zunubansu, [42] zan tuna da alkawarina
da Yaƙub, da alkawarina da Ishaku, da kuma alkawarina da Ibrahim, zan tuna
da ƙasar. [43] Gama za su gudu su bar ƙasar, ƙasar kuwa ta ji daɗin asabbatanta
yayinda take kango muddin ba su ciki. Za su biya hukuncin zunubansu domin
sun ƙi dokokina, suka kuma yi ƙyamar farillaina. [44] Duk da haka, saʼad da suke
a ƙasar abokan gābansu, ba zan ƙi su, ko in yi ƙyamarsu, in hallaka su ƙaƙaf, har in
karya alkawarina da su ba. Ni ne UBANGIJI Allahnsu. [45] Amma saboda su, zan tuna
da alkawarin da na yi da kakanninsu, waɗanda na fitar da su daga Masar a idon
alʼummai, don in zama Allahnsu. Ni ne UBANGIJI.ʼ ”

[46] Waɗannan su ne farillai, da dokoki, da kuma ƙaʼidodin da UBANGIJI ya kafa a
Dutsen Sinai, tsakaninsa da Israʼilawa ta wurin Musa.

# 27

*Fansar abin da yake na UBANGIJI*

1 UBANGIJI ya ce wa Musa, 2 “Ka yi magana da Isra’ilawa, ka ce musu, ‘Duk sa’ad
da mutum ya yi rantsuwa ta musamman zai keɓe wani ga UBANGIJI, ta wurin biyan
kuɗaɗen fansa, 3 ga yadda ma’aunin biyan zai kasance, mutum mai shekara tsakanin
ashirin da sittin, za a biya azurfa hamsin. 4 Mace kuma za a biya azurfa talatin.
5 Saurayi mai shekara tsakanin biyar da ashirin, za a biya azurfa ashirin, yarinya
kuma azurfa goma. 6 Yaro mai shekara tsakanin wata ɗaya da shekara biyar, za a
biya azurfa biyar, ’yar yarinya kuma azurfa uku. 7 Namijin da ya fi shekara sittin, za
a biya azurfa goma sha biyar, mace kuma azurfa goma. 8 In mai alkawarin matalauci
ne da ba zai iya biyan ƙayyadadden abin da aka tsara ba, sai yă tafi wurin firist,
shi firist kuma yă duba yadda mutumin da ya yi alkawarin zai iya biya. Sa’an nan
mutumin zai biya abin da firist ya faɗa.
9 “ ‘In abin da ya yi alkawarin yardajje ne a matsayin hadaya ga UBANGIJI, wannan
dabbar da aka bayar ga UBANGIJI, za tă zama mai tsarki. 10 Kada yă yi musayarta ko
yă yi musaya mai kyau da marar kyau, ko marar kyau da mai kyau; in lalle ne yă yi
musayar dabbar da wata, to, duk wannan da kuma wanda zai yi musayar da ita za
su zama masu tsarki. 11 In abin da ya yi alkawari dabba ce marar tsarki, wadda ba
yardajje ba ce, a matsayin hadaya ga UBANGIJI, dole a kai dabbar wa firist, 12 wanda
zai yanke hukunci dacewarta, ko mai kyau ce, ko marar kyau. Duk darajar da firist
ya kimanta, haka za tă zama. 13 In mai shi yana so yă fanshi dabbar, dole yă ƙara
kashi ɗaya bisa biyar na darajarta.
14 “ ‘In mutum ya miƙa gidansa a matsayin wani abu mai tsarki ga UBANGIJI, firist
zai daidaita dacewar ko mai kyau ne, ko marar kyau. Duk darajar da firist ya kimanta,
haka za tă zama. 15 In mutumin da ya keɓe gidansa ya fanshe shi, dole yă ƙara kashi
ɗaya bisa biyar na darajar, gidan kuma zai zama nasa.
16 “ ‘In wani ya keɓe wa UBANGIJI wani sashe daga cikin gonarsa ta gādo, sai yă
kimanta kuɗin gonar daidai da yawan irin da za a iya shuka a gonar. Za a kimanta
kuɗin a kan shekel hamsin na irin sha’ir. 17 In ya keɓe gonarsa a Shekara ta Murna,
darajar da aka kimanta za tă zauna. 18 Amma in ya keɓe gonar bayan Shekara ta
Murnan, firist zai kimanta darajar bisa ga yawan shekarun da suka rage har zuwa
Shekara ta Murna mai zuwa, sai a rage darajar da aka kimanta a kanta. 19 In mutumin
da ya keɓe gonar, yana so yă fanshe ta, to, dole yă ƙara kashi ɗaya bisa biyar na
darajarta, gonar kuwa tă zama nasa. 20 In kuma bai fanshe gonar ba, ko kuwa in ya
sayar wa wani dabam, ba za a taɓa fanshe ta ba. 21 Sa’ad da aka saki gonar a Shekara
ta Murna, za tă zama mai tsarki, a matsayin gonar da aka miƙa ga UBANGIJI, za tă
zama mallakar firistoci.
22 “ ‘In mutum ya keɓe gonar da ya saya, wadda take ba sashe na gonar iyali ba, ga
UBANGIJI, 23 firist zai kimanta darajarta har Shekara ta Murna, dole kuma mutumin
yă biya darajarta a ranar, a matsayin wani abu mai tsarki ga UBANGIJI. 24 A Shekara
ta Murna ɗin, gonar za tă dawo ga mutumin da aka saye ta daga wurinsa, wanda
yake mai gonar. 25 A kimanta kowace daraja bisa ga ma’aunin shekel na tsattsarkan
wuri, gera ashirin ga shekel.
26 “ ‘Ba wani da zai iya keɓe ɗan farin dabba, da yake ɗan fari ya riga ya zama
na UBANGIJI, ko na saniya, ko na tunkiya, na UBANGIJI ne. 27 In tana cikin dabbobin
da suke marasa tsarki, zai iya saye ta a darajar da aka kimanta, yă ƙara da kashi
ɗaya bisa biyar na darajarta. In bai fanshe ta ba, sai a sayar da ita a darajar da aka
kimanta.
28 “ ‘Amma babu abin da mutum ya mallaka, ya kuma keɓe ga UBANGIJI, ko mutum
ne, ko dabba, ko ganar iyali da za a sayar, ko a fansa; kome da aka keɓe a wannan
hanya, mafi tsarki ne ga UBANGIJI.
29 “ ‘Babu wani da aka keɓe don hallaka da za a fansa; dole a kashe shi.

30 “ ‘Ushirin kome daga gona, ko hatsi daga ƙasa, ko ’ya’yan itatuwa daga itatuwa,
na UBANGIJI ne, mai tsarki ne ga UBANGIJI. 31 In mutum ya fanshi wani zakansa, dole
yă ƙara kashi ɗaya bisa biyar na darajar. 32 Ushirin gaba ɗaya na garken shanu, da
na tumaki, kowane kashi ɗaya bisa goma na dabbar da ta wuce ƙarƙashin sandan
mai kiwo, za tă zama mai tsarki ga UBANGIJI. 33 Kada kuwa ya zaɓa mai kyau daga
marar kyau, ko yă yi musaya. In ya yi musaya kuwa, dabbar da wadda ya musayar,
za su zama masu tsarki, ba kuma za a fanshe su ba.’ ”
34 Waɗannan su ne dokokin da UBANGIJI ya ba wa Musa a Dutsen Sinai saboda
Isra’ilawa.

# Kidaya

*Kidayar yawan mutane*

1 UBANGIJI ya yi magana da Musa a Tentin Sujada a cikin Hamadar Sinai, a rana ta
fari na watan biyu a shekara ta biyu, bayan Isra'ilawa suka fito Masar ya ce, 2 "Ka yi
ƙidayan dukan al'umman Isra'ilawa bisa ga iyalansu da kabilarsu, ka rubuta kowa
da sunansa bi da bi. 3 Da kai da Haruna za ku lissafta dukan mazan Isra'ila bisa ga
sashensu, waɗanda suka kai shekaru ashirin ko fiye, da za su iya shiga soja. 4 Mutum
ɗaya daga kowace kabila wanda yake shugaban danginsa, zai taimake ku.

5 "Ga sunayen da za su taimake ku.

"Daga kabilar Ruben, Elizur ɗan Shedeyur;
6 daga kabilar Simeyon, Shelumiyel ɗan Zurishaddai;
7 daga kabilar Yahuda, Nashon ɗan Amminadab;
8 daga kabilar Issakar, Netanel ɗan Zuwar;
9 daga kabilar Zebulun, Eliyab ɗan Helon;
10 daga kabilar 'ya'yan Yusuf,
daga Efraim, Elishama ɗan Ammihud;
daga Manasse, Gamaliyel ɗan Fedazur;
11 daga kabilar Benyamin, Abidan ɗan Gideyoni;
12 daga kabilar Dan, Ahiyezer ɗan Ammishaddai;
13 daga kabilar Asher, Fagiyel ɗan Okran;
14 daga kabilar Gad, Eliyasaf ɗan Deyuwel;
15 daga kabilar Naftali, Ahira ɗan Enan."

16 Waɗannan su ne mutanen da aka naɗa daga cikin jama'a, shugabannin
asalin kabilu. Su ne kuma shugabannin dangogin Isra'ila.

17 Sai Musa da Haruna suka ɗauki sunayen mutanen nan da aka ba su, 18 suka kira
dukan al'umma wuri ɗaya a rana ta fari ga wata na biyu. Aka kuwa rubuta mutanen
bisa ga asalin kabilansu da iyalansu. Aka kuma rubuta sunayen maza ɗaya-ɗaya
da suka kai shekaru ashirin ko fiye, 19 yadda UBANGIJI ya umarci Musa. Da haka ya
ƙidaya su a Hamadar Sinai.

20 Daga zuriyar Ruben ɗan fari na Isra'ila. Aka rubuta sunayen dukan maza ɗaya-
ɗaya da suka kai shekara ashirin ko fiye da suka isa shiga soja, bisa ga iyalansu
da kabilarsu da take a rubuce. 21 Jimillar maza daga mutanen Ruben 46,500 ne.

22 Daga zuriyar Simeyon. Aka rubuta sunayen dukan maza ɗaya-ɗaya da suka kai
shekara ashirin ko fiye da suka isa shiga soja, bisa ga iyalansu da kabilarsu da
take a rubuce. 23 Jimillar maza daga mutanen Simeyon 59,300 ne.

24 Daga zuriyar Gad. Aka rubuta sunayen dukan maza ɗaya-ɗaya da suka kai
shekara ashirin ko fiye da suka isa shiga soja, bisa ga iyalansu da kabilarsu da
take a rubuce. 25 Jimillar maza daga mutanen Gad 45,650 ne.

26 Daga zuriyar Yahuda. Aka rubuta sunayen dukan maza ɗaya-ɗaya da suka kai
shekara ashirin ko fiye da suka isa shiga soja, bisa ga iyalansu da kabilarsu da
take a rubuce. 27 Jimillar maza daga mutanen Yahuda 74,600 ne.

28 Daga zuriyar Issakar. Aka rubuta sunayen dukan maza ɗaya-ɗaya da suka kai
shekara ashirin ko fiye da suka isa shiga soja, bisa ga iyalansu da kabilarsu da
take a rubuce. 29 Jimillar maza daga mutanen Issakar 54,400 ne.

30 Daga zuriyar Zebulun. Aka rubuta sunayen dukan maza ɗaya-ɗaya da suka kai
shekara ashirin ko fiye da suka isa shiga soja, bisa ga iyalansu da kabilarsu da
take a rubuce. 31 Jimillar maza daga mutanen Zebulun 57,400 ne.

32 Daga ’ya’yan Yusuf.
Daga zuriyar Efraim. Aka rubuta sunayen dukan maza ɗaya-ɗaya da suka kai
shekara ashirin ko fiye da suka isa shiga soja, bisa ga iyalansu da kabilarsu da
take a rubuce. 33 Jimillar maza daga mutanen Efraim 40,500 ne.
34 Daga zuriyar Manasse. Aka rubuta sunayen dukan maza ɗaya-ɗaya da suka kai
shekara ashirin ko fiye da suka isa shiga soja, bisa ga iyalansu da kabilarsu da
take a rubuce. 35 Jimillar maza daga mutanen Manasse 32,200 ne.

36 Daga zuriyar Benyamin. Aka rubuta sunayen dukan maza ɗaya-ɗaya da suka
kai shekara ashirin ko fiye da suka isa shiga soja, bisa ga iyalansu da kabilarsu
da take a rubuce. 37 Jimillar maza daga mutanen Benyamin 35,400 ne.

38 Daga zuriyar Dan. Aka rubuta sunayen dukan maza ɗaya-ɗaya da suka kai
shekara ashirin ko fiye da suka isa shiga soja, bisa ga iyalansu da kabilarsu da
take a rubuce. 39 Jimillar maza daga mutanen Dan 62,700 ne.

40 Daga zuriyar Asher. Aka rubuta sunayen dukan maza ɗaya-ɗaya da suka kai
shekara ashirin ko fiye da suka isa shiga soja, bisa ga iyalansu da kabilarsu da
take a rubuce. 41 Jimillar maza daga mutanen Asher 41,500 ne.

42 Daga zuriyar Naftali. Aka rubuta sunayen dukan maza ɗaya-ɗaya da suka kai
shekara ashirin ko fiye da suka isa shiga soja, bisa ga iyalansu da kabilarsu da
take a rubuce. 43 Jimillar maza daga mutanen Naftali kuwa 53,400 ne.

44 Waɗannan su ne mazan da Musa da Haruna, tare da shugabanni goma
sha biyun nan na Isra’ila suka ƙidaya, kowa a madadin iyalinsa. 45 Dukan
Isra’ilawan da suka kai shekara ashirin ko fiye da suka isa shiga soja, an
ƙidaya su bisa ga iyalansu. 46 Jimillar kuwa ita ce mutum 603,550.

47 Ba a dai ƙidaya zuriyar Lawi tare da saura kabilan ba. 48 Ubangiji ya riga ya
gaya wa Musa cewa, 49 “Ka tabbatar ba ka ƙidaya mutanen Lawi ko kuma ka haɗe
su tare a ƙidayan sauran Isra’ilawa ba. 50 A maimakon haka sai ka naɗa Lawiyawa
su lura da tabanakul Shaida, wato, kan dukan kayayyaki da kuma kome da yake na
wuri mai tsarki. Za su ɗauko tabanakul da dukan kayayyakinsa; za su lura da shi,
su kasance kewaye da shi. 51 Duk sa’ad da za a gusar da tabanakul, Lawiyawa ne za
su saukar da shi; kuma duk sa’ad da za a kafa shi, Lawiyawa ne za su yi haka. Duk
wani dabam da ya je kusa da shi za a kashe shi. 52 Sauran Isra’ilawa za su zauna
ƙungiya-ƙungiya, kowane mutum a ƙungiyarsa daidai bisa ga ƙa’idarsa. 53 Amma

Lawiyawa za su kafa sansaninsu kewaye da tabanakul na Shaida. Don kada fushi yǎ fāɗo a kan al'ummar Isra'ilawa. Hakkin Lawiyawa ne su kula da tabanakul na Shaida."
54 Isra'ilawa suka yi duk waɗannan kamar dai yadda UBANGIJI ya umarci Musa.

# 2

*Tsari yadda kabilu za su zauna a sansani*

1 UBANGIJI ya ce wa Musa da Haruna, 2 "Duk sa'ad da Isra'ilawa suka yi sansani,
kowane mutum zai sauka a inda tutar ƙungiyar kabilarsa take. Sansanin zai kasance a kewaye da Tentin Sujada."

3 Kabilar Yahuda za su yi sansani bisa ga ƙa'idarsu a gabas, wajen fitowar rana. Shugaban mutanen Yahuda kuwa shi ne Nashon ɗan Amminadab.
4 Yawan mutanen sashensa 74,600 ne.
5 Kabilar Issakar za su yi sansani biye da su. Shugabansu shi ne Netanel ɗan Zuwar.
6 Yawan mutanen sashensa 54,400 ne.
7 Kabilar Zebulun za su yi sansani biye da su. Shugabansu shi ne Eliyab ɗan Helon.
8 Yawan mutanen sashensa 57,400 ne.
9 Dukan mazan da aka ba su aiki a sansanin Yahuda bisa ga sashensu sun kai 186,400. Su ne za su ja gaba.

10 A kudu, a nan ne sashe sansanin mutanen Ruben a ƙarƙashin ƙa'idarsu, za su yi sansani. Shugaban mutanen Ruben shi ne Elizur ɗan Shedeyur.
11 Yawan mutanen sashensa 46,500 ne.
12 Kabilar Simeyon za su yi sansani biye da su. Shugaban mutanensa shi ne Shelumiyel ɗan Zurishaddai.
13 Yawan mutanen sashensa 59,300 ne.
14 Kabilar Gad za su zama na biye. Shugaban mutanensa shi ne Eliyasaf ɗan Reyuwel.
15 Yawan mutanen sashensa 45,650 ne.
16 Dukan mazan da aka ba su aiki a sansanin Ruben, bisa ga sashensu sun kai 151,450. Su ne za su zama na biyu in za a tashi.

17 Sa'an nan Lawiyawa ɗauke da Tentin Sujada za su kasance a tsakiyar sansani sa'ad da aka tashi tafiya. Za su kama hanya kamar yadda aka dokace su su zauna a sansani, kowa a wurinsa a ƙarƙashin ƙa'idarsu.

18 Ta wajen yamma kuma sashen Efraim za su yi sansani a ƙarƙashin ƙa'idarsu. Shugaban mutanensa, shi ne Elishama ɗan Ammihud.
19 Yawan mutanen sashensa 40,500 ne.
20 Kabilar Manasse ce za tǎ zama ta biye. Shugabansu shi ne Gamaliyel ɗan Fedazur.
21 Yawan mutanen sashensa 32,200 ne.
22 Na biye da su su ne mutanen Benyamin. Shugaban mutanensu kuwa Abidan ɗan Gideyoni.
23 Yawan mutanen sashensa 35,400 ne.
24 Dukan mazan da aka ba su aiki a sansanin Efraim, bisa ga sashensu su kai 108,100 ne. Su ne za su zama na uku sa'ad da za a tashi.

25 A arewa za a sami sashen sansanin Dan, a ƙarƙashin ƙa'idarsu. Shugabansu shi ne Ahiyezer ɗan Ammishaddai.
26 Yawan mutanen sashensa 62,700 ne.
27 Kabilar Asher ce za tǎ zama ta biye. Shugabansu shi ne Fagiyel ɗan Okran.
28 Yawan mutanen sashensa 41,500 ne.

29 Kabilar Naftali za su zama na biye da su. Shugaban mutanen kuwa shi ne Ahira
ɗan Enan. 30 Yawan mutanen sashensa 53,400 ne
31 Dukan mazan da aka ba su aiki a sansanin Efraim, bisa ga sashensu su kai
157,600. Su ne za su zama na ƙarshe, ƙarƙashin ƙa'idarsu.

32 Waɗannan su ne Isra'ilawan da aka a ƙidaya bisa ga iyalansu. Dukansu
da suke a sansani, mutane 603,550 ne. 33 Ba a dai ƙidaya Lawiyawa tare
da sauran Isra'ilawa ba yadda UBANGIJI ya umarci Musa.

34 Saboda haka Isra'ilawa suka yi duk ko mene ne da UBANGIJI ya umarci Musa.
Ta haka ne suka yi sansani a ƙarƙashin ƙa'idarsu kowanne tare da kabilarsa da
danginsa.

# 3

*Lawiyawa*

1 Waɗannan su ne zuriyar Haruna da Musa a lokacin da UBANGIJI ya yi magana da
Musa a kan Dutsen Sinai.

2 Sunayen 'ya'yan Haruna su ne, Nadab ɗan fari, da Abihu, da Eleyazar da Itamar.
3 Waɗannan su ne sunayen 'ya'yan Haruna, shafaffun firistocin da aka naɗa domin
su yi aiki firist. 4 Amma Nadab da Abihu suka fāɗi suka mutu a gaban UBANGIJI a
Hamadar Sinai a sa'ad da suka ƙona turare da haramtacciyar wuta a gabansa. Ba su
kuwa da 'ya'ya; saboda haka Eleyazar da Itamar kaɗai suka yi aiki firist a zamanin
mahaifinsu Haruna.
5 UBANGIJI ya ce wa Musa, 6 "Ka kawo mutanen Lawi, ka kuma gabatar da su
ga Haruna firist, don su taya shi aiki. 7 Za su yi wa Haruna da dukan al'umma
aikace-aikace a Tentin Sujada, ta wurin yin aikin tabanakul. 8 Za su lura da dukan
kayayyakin Tentin Sujada, suna cika hakkin Isra'ilawa ta wurin yin aiki a tabanakul.
9 Ka ba da Lawiyawa ga Haruna da 'ya'yansa; su ne za su zama Isra'ilawan da za a
ba da su ɗungum gare shi. 10 Ka naɗa Haruna da 'ya'yansa su yi aiki firistoci; duk
wanda ya yi shisshigi a wuri mai tsarki kuwa dole a kashe shi."
11 UBANGIJI ya kuma ce wa Musa, 12 "Ga shi na ɗauki Lawiyawa daga cikin Isra'ilawa
a maimakon ɗan fari na kowace mace a Isra'ila. Lawiyawa nawa ne, 13 gama duk
'ya'yan fari nawa ne. Lokacin da karkashe duk 'ya'yan fari a Masar, na keɓe wa
kaina kowane ɗan fari a Isra'ila, ko mutum, ko dabba. Za su zama nawa. Ni ne
UBANGIJI."
14 UBANGIJI ya yi magana da Musa a Hamadar Sinai ya ce, 15 "Ka ƙidaya Lawiyawa
bisa ga iyalansu da kabilarsu. Ka ƙidaya kowane ɗan jinjiri mai wata ɗaya ko fiye."
16 Saboda haka Musa ya ƙidaya su duka, kamar yadda maganar UBANGIJI ta umarta.

17 Ga sunayen 'ya'yan Lawi,
Gershon, Kohat da Merari.
18 Ga sunayen mutanen Gershon,
Libni, da Shimeyi
19 Sunayen mutanen Kohat kuwa su ne,
Amram, Izhar, Hebron da Uzziyel.
20 Dangin Merari su ne.
Mali da Mushi.

Ga kabilan Lawiyawa bisa ga iyalansu.

21 A wajen Gershonawa, kabilarsa su ne Libniyawa, da Shimeyiyawa; waɗannan su ne mutanen Gershom.
22 Jimillar dukan jarirai maza daga wata ɗaya zuwa gaba da haihuwa su kai 7,500.
23 Kabilar Gershonawa za su yi sansani ta fuskar yamma, a bayan tabanakul.
24 Eliyasaf ɗan Layel shi ne shugaban iyalan Gershonawa.
25 A Tentin Sujada, Gershonawa su ne za su lura da mazauni da tabanakul da kuma
tentin, abubuwan rufensa, labule a ƙofar Tentin Sujada, 26 da labulen filin da yake
kewaye da tabanakul da kuma bagade, da igiyoyi, da kuma kowane abin da ya danganci aikinsu.

27 Kabilar Kohat su ne, Amramawa da Izharawa da Hebronawa da Uzziyelawa; waɗannan su ne kabilar Kohatawa.
28 Jimillar dukan jarirai maza daga wata ɗaya ko fiye, 8,600 ne.
Kohatawa ne suke lura da wuri mai tsarki.
29 Kohatawa za su yi sansani a kudu da tabanakul.
30 Shugaban kabilar Kohatawa shi ne Elizafan ɗan Uzziyel.
31 Su ne da hakkin kula da akwatin alkawari, tebur, wurin ajiye fitila, bagade, kayayyakin wuri mai tsarki da ake amfani da su a sujada, labule, da kuma kome da ya danganci aikinsu.
32 Babban shugaban Lawiyawa shi ne Eleyazar ɗan Haruna, firist. An naɗa shi a kan waɗanda suke kula da wuri mai tsarki.

33 Kabilar Merari su ne Maliyawa da Mushiyawa; waɗannan su ne kabilar Merari.
34 Jimillar dukan jarirai maza daga wata ɗaya ko fiye, 6,200 ne.
35 Shugaban iyalan Merari shi ne Zuriyel ɗan Abihayil.
Za su yi sansani arewa da tabanakul.
36 Kabilar Merari ne aka sa su lura da katakan tabanakul, sandunanta, dogayen sandunanta, tarukanta, dukan kayan aiki da kowane abin da ya danganci aikinsu,
37 da ginshiƙai kewaye da filin tare da rammuka da turaku da igiyoyinsu.

38 Musa da Haruna da ʼyaʼyansu za su yi sansani gabas da tabanakul, wajen fitowar rana; a gaban Tentin Sujada.
Su ne da hakkin lura da wuri mai tsarki a madadin Israʼilawa.
Duk wani wanda ba ya wannan aiki, ya kuma kusaci wuri mai tsarki, za a kashe shi.

39 Jimillar Lawiyawan da Musa da Haruna suka ƙidaya bisa ga umarnin Ubangiji bisa ga danginsu, haɗe da kowane jariri daga wata ɗaya ko fiye, 22,000 ne.

40 Sai Ubangiji ya ce wa Musa, “Kidaya dukan ʼyaʼyan fari na Israʼilawa maza daga
wata ɗaya da kuma fiye ka kuma rubuta sunayensu. 41 Ka ɗauko mini Lawiyawa
a maimakon dukan ʼyaʼyan fari na Israʼilawa, haka ma na dabbobi na Lawiyawa, a maimakon ʼyaʼyan fari na dabbobin Israʼilawa. Ni ne Ubangiji.”
42 Haka Musa ya ƙidaya ʼyaʼyan fari na Israʼilawa, yadda Ubangiji ya umarce shi.
43 Jimillar ʼyaʼyan fari maza daga wata ɗaya da kuma fiye, da aka rubuta bisa ga sunayensu, 22,273 ne.
44 Sai Ubangiji ya kuma yi magana da Musa ya ce, 45 “Ka ɗauki Lawiyawa a
maimakon dukan ʼyaʼyan fari na Israʼila, dabbobin Lawiyawa kuma a maimakon
dabbobinsu. Lawiyawa za su zama nawa. Ni ne Ubangiji. 46 Don a fanshi ʼyaʼyan

fari 273 na Isra'ilawa da suka fi Lawiyawa yawa, [47] ka karɓi shekel biyar domin
kowannensu, bisa ga ma'aunin shekel na tsattsarkan wuri, wanda yake da nauyin
gera ashirin. [48] Ka ba wa Haruna da 'ya'yansa kuɗin fansar da ya haura kai na
'ya'yan farin Isra'ilawa."

[49] Haka, Musa ya karɓi kuɗin fansar waɗanda suka haura yawan Lawiyawa.
[50] Daga 'ya'yan fari na Isra'ilawa, ya karɓi azurfa masu nauyin shekel 1,365, bisa
ga ma'aunin shekel na tsattsarkan wuri. [51] Sa'an nan Musa ya ba da kuɗin fansar ga
Haruna da 'ya'yansa, yadda maganar UBANGIJI ta umarce shi.

# 4

*Kohatawa*

[1] UBANGIJI ya ce wa Musa da Haruna, [2] "Ku yi ƙidaya Kohatawa daga Lawiyawa,
bisa ga kabilarsu da iyalansu. [3] Ku ƙidaya dukan maza daga shekara talatin zuwa
hamsin da suka zo domin aiki a Tentin Sujada.

[4] "Ga aikin Kohatawa a Tentin Sujada, kulawa da kayayyaki mafi tsarki. [5] Lokacin
da za a tashi daga sansani, Haruna da 'ya'yansa za su shiga ciki su kunce labulen
kāriya, su rufe Akwatin Alkawari da shi. [6] Sa'an nan su rufe shi da fatun shanun
teku, su shimfiɗa zane mai ruwan shuɗi a bisansa, su sa masa sandunansa.

[7] "A bisa teburin Burodin Ajiyewa, za su shimfiɗa zane mai ruwan shuɗi, a kansa
kuma su sa farantai, kwanoni da manyan kwanoni, da tuluna don hadayun sha; da
burodin da zai ci gaba da kasancewa a kansa. [8] A bisa waɗannan za su shimfiɗa jan
zane, su rufe su da fatun shanun teku, su kuma zura masa sandunansa.

[9] "Za su ɗauki zane mai ruwan shuɗi su rufe wurin ajiye fitilan da yake don fitilu,
tare da fitilunsa, lagwaninsa da farantansa, da dukan tulunansa don man amfaninsu.
[10] Sa'an nan su naɗe shi da kuma dukan kayayyakinsa a cikin fatar shanun teku, su
sa shi a kan sandan ɗaukarsa.

[11] "A kan bagaden zinariya, za su shimfiɗa zane mai ruwan shuɗi, su kuma rufe
shi da fatar shanun teku, sai a zura masa sandunansa.

[12] "Za su ɗauki dukan kayayyakin da ake amfani da su a wuri mai tsarki, su
nannaɗe su da zane mai ruwan shuɗi, su rufe shi da fatar shanun teku, sa'an nan a
sa su a kan sandan ɗaukarsa.

[13] "Za su kwashe tokar da take a bagaden tagulla, su shimfiɗa zane mai ruwan
shuɗi a bisansa. [14] Sa'an nan su sa a kansa dukan kayayyakin da aka yi amfani da su
a bagaden, haɗe da farantai don wuta, cokula masu yatsu don nama, manyan cokula,
da darunan yayyafawa. A kansa za su shimfiɗa murfi na fatun shanun teku, su zura
sandunan ɗaukarsa.

[15] "Bayan Haruna da 'ya'yansa suka gama rufe kayayyaki masu tsarki da dukan
abubuwa masu tsarki, sa'ad da kuma aka shirya tashi daga sansani, sai Kohatawa su
zo gaba, su ɗauka. Amma kada su taɓa abubuwa masu tsarki, don kada su mutu.
Kohatawa za su ɗauki abubuwan da suke cikin Tentin Sujada.

[16] "Eleyazar ɗan Haruna firist zai lura da man fitila da turare da hadaya ta gari na
kullum da kuma keɓaɓɓen mai. Shi ne zai lura da dukan tabanakul da duk abin da
yake cikinsa da kuma kayayyaki da abubuwan masu tsarki."

[17] UBANGIJI ya ce wa Musa da Haruna, [18] "Ku tabbata cewa ba a kawar da zuriyar
Kohatawa daga Lawiyawa ba. [19] Saboda su rayu, kada su mutu sa'ad da suka zo
kusa da abubuwa mafi tsarki, a yi musu wannan, wato, Haruna da 'ya'yansa za su
shiga wuri mai tsarki su ba wa kowane mutum aikinsa da kuma abin da zai ɗauka.
[20] Amma kada Kohatawa su shiga don su dubi abubuwa masu tsarki, ko na ɗan
ƙanƙanin lokaci, in ba haka ba za su mutu."

*Gershonawa*

21 Ubangiji ya ce wa Musa, 22 “Ka ƙidaya mutanen Gershon bisa ga iyalansu da
kabilarsu. 23 Ka ƙidaya maza masu shekara talatin zuwa hamsin waɗanda sukan zo
hidimar aiki a Tentin Sujada.
24 “Ga aikin kabilar Gershonawa yayinda suke aiki, suke kuma ɗaukar kaya. 25 Za
su ɗauki labulen tabanakul, Tentin Sujada, kayan da za a rufe shi, da kuma kayan
da za a rufe shi daga waje na fatun rufuwa na shanun teku, labulen ƙofar Tentin
Sujada, 26 labulen filin da yake kewaye da tabanakul da bagade, labulen ƙofa, igiyoyi
da kuma dukan abubuwan da ake amfani da su wajen hidima. Geshonawa za su yi
dukan abin da ya kamata a yi da waɗannan abubuwa. 27 Dukan hidimominsu, ko na
ɗauko, ko kuma na yin wani aiki, za a yi su ne bisa ga umarnin Haruna da 'ya'yansa.
Za ka ba su dukan kayan da za su ɗauka a matsayin hakkinsu. 28 Wannan shi ne
hidimar da kabilar Gershonawa za su yi a Tentin Sujada. Ayyukansu za su kasance
bisa ga umarnin Itamar ɗan Haruna firist.

### *Merariyawa*

29 “Ka ƙidaya kabilar Merari bisa ga kabilarsu da iyalansu. 30 Ka ƙidaya maza
daga masu shekara talatin zuwa hamsin waɗanda sukan zo hidimar aiki a Tentin
Sujada. 31 Ga aikinsu sa'ad da suke hidima a Tentin Sujada, za su ɗauki katakan
tabanakul, sandunansa da dogayen sandunansa, da rammukansa, 32 har ma da
dogayen sandunan kewayen filin da rammukansu, turakun tenti, igiyoyi, da dukan
kayayyaki, da kuma dukan abubuwan da suke dangane da amfaninsu. Ka ba wa
kowane mutum ayyuka na musamman da zai yi. 33 Wannan ce hidimar da mutanen
Merari za su yi a aikin Tentin Sujada, a ƙarƙashin jagorancin Itamar ɗan Haruna,
firist.”

### *Kidayar kabilar Lawiyawa*

34 Musa, Haruna da kuma shugabannin jama'a, suka ƙidaya Kohatawa ta kabilarsu
da kuma iyalansu. 35 Dukan maza daga shekara talatin zuwa hamsin waɗanda sukan
zo hidimar aiki a Tentin Sujada, 36 da aka ƙidaya, kabila-kabila, su 2,750 ne. 37 Jimillar
dukan waɗanda suke na kabilan Kohatawa, waɗanda suka yi hidimar aiki a Tentin
Sujada ke nan. Musa da Haruna sun ƙidaya su bisa ga umarnin Ubangiji.

38 Aka ƙidaya mazan Gershonawa ta kabilansu da kuma iyalansu. 39 Dukan maza
daga shekara talatin zuwa hamsin waɗanda sukan zo hidimar aiki a Tentin Sujada,
40 da aka ƙidaya kabila-kabila da kuma iyali-iyali, su 2,630 ne. 41 Jimillar waɗanda
suke na kabilar Gershonawa ke nan, waɗanda suka yi hidimar aiki a Tentin Sujada.
Musa da Haruna sun ƙidaya su bisa ga umarnin Ubangiji.

42 Aka ƙidaya mazan Merari ta kabilarsu da kuma iyalansu. 43 Dukan maza daga
shekara talatin zuwa hamsin waɗanda sukan zo hidimar aiki a Tentin Sujada, 44 da
aka ƙidaya kabila-kabila, su 3,200 ne. 45 Jimillar waɗanda suke na kabilar Merari ke
nan. Musa da Haruna suka ƙidaya su bisa ga umarnin Ubangiji.
46 Saboda haka, Musa, Haruna da shugabannin Isra'ila, suka ƙidaya dukan
Lawiyawa kabila-kabila da kuma iyali-iyali. 47 Dukan maza daga shekara talatin zuwa
hamsin waɗanda sukan zo hidimar aiki da kuma ɗaukar Tentin Sujada 48 jimillarsu
ta kai 8,580. 49 Bisa ga umarnin Ubangiji ta wurin Musa, aka ba kowa aikinsa, aka
kuma faɗa musu abin da za su ɗauka.

Ta haka aka ƙidaya su, yadda Ubangiji ya umarci Musa.

# 5

*Tsabtaccewar sansani*

1 UBANGIJI ya ce wa Musa, 2 “Ka umarci Isra’ilawa su kori duk wanda yake da ciwon
fatan jiki, ko mai ɗiga na kowane iri, ko wanda ya ƙazantu ta wurin taɓa gawa, daga
cikin sansani. 3 Ka kori maza da mata ma; ka kai su bayan sansani domin kada su
ƙazantar da sansani inda nake zama a cikinsu.” 4 Isra’ilawa suka yi haka; suka kore
su daga sansanin. Suka aikata yadda dai UBANGIJI ya umarci Musa.

*Biyan diyya saboda abin da aka yi ba daidai ba*
*(Firistoci 6.1-7)*

5 UBANGIJI ya ce wa Musa, 6 “Gaya wa Isra’ilawa, ‘Sa’ad da namiji ko mace ya yi
wa ɗan’uwansa laifi ta kowace hanya, ta yin haka, ya yi rashin aminci ga UBANGIJI,
mutumin kuwa ya yi laifi ke nan 7 kuma dole yă furta zunubin da ya yi. Dole yă
yi biya cikakkiyar diyya saboda laifinsa, yă ƙara kashi ɗaya bisa biyar a kai, yă
kuma bayar da shi duka ga wanda ya yi wa laifin. 8 Amma in mutumin da aka yi
wa laifin ba shi da ɗan’uwa na kusa da za a biya diyya saboda laifin, sai diyyar tă
zama ta UBANGIJI, dole kuma a ba wa firist, haɗe da ragon da za a yi kafara da shi.
9 Dukan tsarkakakkun abubuwan da Isra’ilawa suka kawo wa firist za su zama nasa.
10 Kowace tsarkakakkiyar kyauta da mutum ya kawo nasa ne, sai dai abin da ya ba
wa firist, zai zama na firist.’ ”

*Gwaji don mace marar aminci*

11 Sai UBANGIJI ya ce wa Musa, 12 “Yi magana da Isra’ilawa, ka ce musu, ‘In matar
wani ta kauce, ta kuma yi rashin aminci gare shi 13 ta wurin kwana da wani dabam,
wannan kuwa ya kasance a ɓoye ga mijinta, rashin tsarkinta kuwa bai tonu ba (da
yake babu shaida, ba a kuma kama ta tana yi ba), 14 in kuma kishi ya sha kan mijinta
kuma tana da ƙazanta, ko kuwa idan yana kishi yana kuma zatonta ko ma ba ta da
ƙazanta 15 mijin zai kai matansa a gaban firist, yă kuma kawo hadayar abubuwan
da ake bukata; abubuwa kamar, garin sha’ir garwa ɗaya, amma kada yă zuba mai
a kan garin sha’ir, kada kuma yă sa turaren wuta a kansa, domin hadaya ce ta miji
mai tuhumar matarsa da aka kawo domin gaskiya tă fito fili.
16 “ ‘Firist zai kawo ta, yă sa tă tsaya a gaban UBANGIJI. 17 Sa’an nan zai ɗebi ruwa
mai tsarki a tulun laka, yă zuba ƙurar da ya ɗebo daga daɓen tabanakul a cikin
ruwan. 18 Bayan da firist ya sa matan ta tsaya a gaban UBANGIJI, sai yă kunce gashin
kanta, yă kuma sa hadaya ta gari don tunawa a hannuwanta, hadayar gari ce ta kishi,
yayinda shi kansa zai riƙe ruwa mai ɗaci, mai jawo la’ana. 19 Sa’an nan firist zai sa
tă yi rantsuwa, yă kuma ce mata, “In ba wani mutumin da ya kwana da ke kuma ba
ki kauce kin ƙazantar da kanki yayinda kike auren mijinki ba, kada wannan ruwa
mai ɗaci, mai jawo la’ana, yă cuce ki. 20 Amma in kin kauce yayinda kike auren
mijinki, kika kuma ƙazantar da kanki ta wurin kwana da wani dabam da ba mijinki
ba,” 21 (a nan firist zai sa macen a ƙarƙashin la’anar rantsuwa cewa) “bari UBANGIJI
yă sa mutanenki su la’ance ki, su kuma yi Allah wadai da ke, sa’ad da UBANGIJI ya sa
cinyarki ta shanye, cikinki kuma ya kumbura. 22 Bari wannan ruwa mai jawo la’ana,
yă shiga jikinki saboda cikinki yă kumbura, cinyarki kuma yă shanye.”
“ ‘Sai macen tă ce, “Amin. Bari yă zama haka.”
23 “ ‘Firist zai rubuta waɗannan la’anoni a littafi, sa’an nan yă wanke su cikin ruwa
mai ɗaci. 24 Sai yă sa macen tă sha ruwa mai ɗaci, mai jawo la’ana, wannan ruwa
kuwa zai shiga cikinta yă kawo mata wahala mai zafi. 25 Firist zai karɓi hadaya ta
gari don kishi daga hannuwanta, yă kaɗa shi a gaban UBANGIJI sa’an nan yă kawo a
bagade. 26 Sa’an nan firist zai ɗiba hatsi na hadaya cike da hannunsa don hadayar
tunawa, yă kuma ƙone a bagade; bayan haka sai yă sa macen tă sha ruwan. 27 In

ta ƙazantar da kanta ta kuma ci amanar mijinta, to, yayinda aka sa tă sha ruwa
mai jawo la’ana, ruwan zai shiga cikinta, yă jawo mata wahala mai zafi; cikinta zai
kumbura, cinyarta kuma yă shanye, tă kuwa zama la’ananniya a cikin mutanenta.
28 Amma fa, in macen ba tă ƙazantar da kanta ba, ba tă kuma da ƙazanta, za a
kuɓutar da ita daga laifin, za tă kuma iya haihuwa.
29 “ ‘Wannan dai, ita ce dokar kishi sa’ad da mace ta kauce, ta kuma ƙazantar
da kanta yayinda take aure da mijinta, 30 ko kuma sa’ad da mijin yana kishi domin
yana shakkar matarsa. Firist zai sa tă tsaya a gaban UBANGIJI, yă kuma yi amfani
da wannan doka gaba ɗaya a kanta. 31 Mijin zai zama marar laifi daga kowane laifi,
amma matar za tă ɗauki muguntarta, idan ta yi laifin.’ ”

# 6

*Banazare*

1 UBANGIJI ya ce wa Musa, 2 “Yi magana da Isra’ilawa, ka ce musu, ‘In mace, ko
namiji yana so yă yi alkawari na musamman, alkawarin zaman keɓaɓɓe ga UBANGIJI,
a matsayin Banazare, 3 dole yă keɓe kansa daga ruwan inabi, ko daga waɗansu
abubuwa sha masu sa maye, kada kuma yă sha ruwan tsamin da aka yi daga ruwan
inabi, ko daga waɗansu abubuwa sha masu sa maye. Ba zai sha ruwan ’ya’yan inabi,
ko yă ci ’ya’yan inabi ɗanye ko busasshe ba. 4 Muddin yana Banazare, ba zai ci wani
abin da ya fito daga ’ya’yan inabi ba, ko ƙwayar inabi, ko ɓawonsa ma.
5 “ ‘A dukan lokacin da yake a kan alkawarin keɓewarsa, reza ba zai taɓa kansa.
Dole yă kasance da tsarki har ƙarshen keɓewarsa ga UBANGIJI; tilas yă bar gashin
kansa yă yi tsawo. 6 A dukan kwanakin keɓewarsa ga UBANGIJI, Banazarin ba zai yi
kusa da gawa ba. 7 Ko da ma gawar ta mahaifinsa ce, ko ta mahaifiyarsa, ko ta ɗan
mahaifiyarsa, ko kuma ta ’yar’uwarsa ce, ba zai ƙazantar da kansa saboda su ba,
domin alamar keɓewarsa ga Allah tana kansa. 8 A dukan kwanakin keɓewarsa, an
tsarkake shi ga UBANGIJI.
9 “ ‘In farat ɗaya wani ya mutu kusa da shi, to, keɓewarsa ta ƙazantu, dole yă aske
kansa a ranar tsarkakewarsa, a rana ta bakwai. 10 Sa’an nan a rana ta takwas, tilas yă
kawo wa firist ’yan kurciyoyi biyu, ko kuma ’yan tattabarai biyu a bakin ƙofar Tentin
Sujada. 11 Firist kuwa zai miƙa ɗaya don hadaya ta zunubi, ɗayan kuma don hadaya
ta ƙonawa, yă yi kafara dominsa, gama ya yi zunubi ta dalilin gawar. A wannan rana
zai sāke keɓe kansa. 12 Dole yă keɓe kansa ga UBANGIJI, har kwanakin keɓewarsa,
kuma dole yă kawo ɗan rago bana ɗaya a matsayin hadayar laifi. Kwanakin baya ba
sa cikin lissafi, domin ya ƙazantu a lokacin keɓewarsa.
13 “ ‘To, ga doka saboda Banazare sa’ad da kwanakin keɓewarsa suka gama. Za
a kawo shi a bakin ƙofar Tentin Sujada. 14 A can zai miƙa hadayunsa ga UBANGIJI.
Hadayun kuwa su ne, ɗan rago, bana ɗaya marar lahani don hadaya ta ƙonawa,
’yar tunkiya, bana ɗaya marar lahani na hadaya don zunubi, rago marar lahani don
hadaya ta salama, 15 tare da hadayu na hatsi da hadayu na sha, da kuma kwando
burodi marar yisti, ƙosai da aka yi da lallausan gari kwaɓaɓɓe da mai, da kuma
wainan da aka barbaɗa da mai.
16 “ ‘Firist zai kawo su a gaban UBANGIJI, yă miƙa hadaya don zunubi da hadaya ta
ƙonawa. 17 Zai miƙa kwandon burodi marar yisti, yă kuma miƙa ɗan ragon hadaya
ta salama tare da hadaya ta gari, da hadaya ta sha ga UBANGIJI.
18 “ ‘Sa’an nan a ƙofar Tentin Sujada, dole Banazaren yă aske gashin da ya alamta
keɓewarsa, yă kwashe gashin, yă zuba a cikin wutar da take ƙarƙashin hadaya ta
salama.
19 “ ‘Bayan Banazaren ya aske gashinsa da ya alamta keɓewa, firist zai ɗauki
dafaffiyar kafaɗar rago, da ƙosai da kuma waina daga cikin kwando waɗanda duka

biyu marar yisti ne, yǎ sa su a tafin hannun keɓaɓɓen. 20 Firist zai kaɗa su a gaban
UBANGIJI, hadaya ce ta kaɗawa; mai tsarki ne kuma, zai zama na firist, tare da ƙirjin
da aka kaɗa da kuma cinyar da aka kawo. Bayan haka, Banazaren zai iya shan ruwan
inabi.
21 " 'Wannan ita ce dokar Banazare wanda ya yi alkawari ga UBANGIJI bisa ga
keɓewarsa, tare da duk abin da zai iya bayarwa. Tilas yǎ cika alkawarin da ya yi
bisa ga dokar zaman Banazare.' "

### *Albarkar da firist zai sa wa jama'a*

22 UBANGIJI ya ce wa Musa, 23 "Gaya wa Haruna da 'ya'yansa, 'Ga yadda za ku
albarkaci Isra'ilawa. Za ku ce musu,
24 " ' "UBANGIJI yǎ albarkace ku,
yǎ kuma kiyaye ku;
25 UBANGIJI yǎ sa fuskarsa ta haskaka a kanku,
yǎ kuma yi muku alheri;
26 UBANGIJI yǎ dube ku da idon rahama,
yǎ kuma ba ku salama." '
27 "Da haka za su sa sunana a kan Isra'ilawa, ni kuma zan albarkace su."

# 7

### *Hadayu a keɓewar tabanakul*

1 Sa'ad da Musa ya gama kafa tabanakul, sai ya shafe shi da mai, ya tsarkake shi
tare da dukan kayayyakinsa, ya kuma shafe bagaden da mai, ya tsarkake shi da dukan
kayayyakinsa. 2 Sa'an nan shugabannin Isra'ila, wato, shugabannin iyalai waɗanda
suke shugabancin kabilan da aka ƙidaya, suka miƙa hadayu. 3 Suka kawo kyautansu
a gaban UBANGIJI. Kyautayin kuwa su ne, kekunan yaƙi shida da aka rufe, da shanu
goma sha biyu, saniya guda daga kowane shugaba, da kuma keken yaƙi guda daga
shugabanni biyu. Suka miƙa waɗannan a gaban tabanakul.
4 UBANGIJI ya ce wa Musa, 5 "Ka karɓi abubuwan nan daga gare su, domin a yi
amfani da su a aikin Tentin Sujada. Ka ba da su ga Lawiyawa, a ba kowane mutum
bisa ga aikinsa."
6 Haka fa Musa ya ɗauki kekunan yaƙi da shanun ya ba wa Lawiyawa. 7 Ya ba wa
Gershonawa, kekunan yaƙi biyu da shanu huɗu bisa ga aikinsu, 8 ya kuma ya ba wa
kabilar Merari kekunan yaƙi huɗu da shanu takwas bisa ga aikinsu. Aka ba da su
duka a ƙarƙashin ikon Itamar ɗan Haruna, firist. 9 Amma Musa bai ba wa Kohatawa
kome ba, gama aikinsu shi ne lura da kayayyaki masu tsarki waɗanda ake ɗauka a
kafaɗa.
10 Sa'ad da aka shafe bagaden da mai, sai shugabannin suka kawo hadayunsu
saboda keɓewarsa, suka miƙa su a bagaden. 11 Gama UBANGIJI ya riga ya gaya
wa Musa cewa, "Kowace rana, shugaba guda zai kawo hadayarsa saboda keɓewar
bagade."

12 Wanda ya kawo hadayarsa a rana ta farko shi ne Nashon ɗan Amminadab,
shugaban mutanen Yahuda.
13 Hadayar da ya kawo ita ce,
faranti guda ɗaya na azurfa, nauyinsa shekel ɗari ɗaya da talatin, da kuma daro
na yayyafawa na azurfa, nauyinsa shekel saba'in, dukan biyu, an auna su bisa
ga ma'aunin shekel na tsattsarkan wuri ne, kowannensu cike da lallausan gari,
haɗe da mai kamar hadaya ta gari;
14 ya kawo kwanon zinariya ɗaya, mai nauyin shekel goma, cike da turaren
hayaƙi;

15 da ƙaramin bijimi guda ɗaya, tunkiya ɗaya, da rago, dukansu bana ɗaya-ɗaya domin hadaya ta ƙonawa;
16 ya kuma kawo bunsuru ɗaya domin hadaya don zunubi;
17 da shanu biyu, raguna biyar, bunsurai biyar da kuma ʼyan raguna biyar dukansu bana ɗaya-ɗaya, a miƙa su hadaya ta salama.
Wannan ita ce hadayar Nashon ɗan Amminadab.

18 A rana ta biyu, Netanel ɗan Zuwar, shugaban mutanen Issakar, ya kawo hadayarsa.
19 Hadayar da ya kawo ita ce,
faranti guda ɗaya na azurfa, nauyinsa shekel ɗari ɗaya da talatin, da kuma daro na yayyafawa na azurfa, nauyinsa shekel sabaʼin, dukan biyu, an auna su bisa ga maʼaunin shekel na tsattsarkan wuri, kowannensu cike da lallausan gari, haɗe da mai kamar hadaya ta gari;
20 ya kuma kawo kwanon zinariya ɗaya mai nauyin shekel, goma cike da turaren hayaƙi;
21 da ƙaramin bijimi guda ɗaya, tunkiya ɗaya da rago, dukansu bana ɗaya-ɗaya domin hadaya ta ƙonawa;
22 ya kuma kawo bunsuru ɗaya domin hadaya don zunubi;
23 da shanu biyu, raguna biyar, bunsurai biyar da kuma ʼyan raguna biyar dukansu bana ɗaya-ɗaya, a miƙa su hadaya ta salama.
Wannan ita ce hadayar Netanel ɗan Zuwar.

24 A rana ta uku, Eliyab ɗan Helon, shugaban mutanen Zebulun, ya kawo hadayarsa.
25 Hadayar da ya kawo ita ce,
faranti guda ɗaya na azurfa, nauyinsa shekel ɗari ɗaya da talatin, da kuma daro na yayyafawa na azurfa, nauyinsa shekel sabaʼin, dukan biyu, an auna su bisa ga maʼaunin shekel na tsattsarkan wuri, kowannensu cike da lallausan gari, haɗe da mai kamar hadaya ta gari;
26 ya kuma kawo kwanon zinariya ɗaya, mai nauyin shekel goma, cike da turaren hayaƙi;
27 da ƙaramin bijimi guda ɗaya, tunkiya ɗaya, da rago, dukansu bana ɗaya-ɗaya domin hadaya ta ƙonawa;
28 ya kuma kawo bunsuru ɗaya domin hadaya don zunubi;
29 da shanu biyu, raguna biyar, bunsurai biyar da kuma ʼyan raguna biyar, dukansu bana ɗaya-ɗaya, a miƙa su hadaya ta salama.
Wannan ita ce hadayar Eliyab ɗan Helon.

30 A ranan ta huɗu, Elizur ɗan Shedeyur, shugaban mutanen Ruben, ya kawo hadayarsa.
31 Hadayar da ya kawo ita ce,
faranti guda ɗaya na azurfa, nauyinsa shekel ɗari ɗaya da talatin, da kuma daro na yayyafawa na azurfa, nauyinsa shekel sabaʼin, dukan biyu, an auna su bisa ga maʼaunin shekel na tsattsarkan wuri, kowannensu cike da lallausan gari, haɗe da mai kamar hadaya ta gari;
32 ya kuma kawo kwanon zinariya ɗaya mai nauyin shekel goma, cike da turaren hayaƙi;
33 da ƙaramin bijimi guda ɗaya, tunkiya ɗaya, da rago, dukansu bana ɗaya-ɗaya domin hadaya ta ƙonawa;

34 ya kuma kawo bunsuru ɗaya domin hadaya don zunubi;
35 da shanu biyu, raguna biyar, bunsurai biyar da kuma ʼyan raguna biyar,
dukansu bana ɗaya-ɗaya, a miƙa su hadaya ta salama.
Wannan ita ce hadayar Elizur ɗan Shedeyur.

36 A rana ta biyar, Shelumiyel ɗan Zurishaddai, shugaban mutanen Simeyon,
ya kawo hadayarsa.
37 Hadayar da ya kawo ita ce,
faranti guda ɗaya na azurfa, nauyinsa shekel ɗari ɗaya da talatin, da kuma daro
na yayyafawa na azurfa, nauyinsa shekel sabaʼin, dukan biyu, an auna su bisa
ga maʼaunin shekel na tsattsarkan wuri, kowannensu cike da lallausan gari,
haɗe da mai kamar hadaya ta gari;
38 ya kuma kawo kwanon zinariya ɗaya mai nauyin shekel goma, cike da turaren
hayaƙi;
39 da ƙaramin bijimi guda ɗaya, tunkiya ɗaya, da rago, dukansu bana ɗaya-ɗaya
domin hadaya ta ƙonawa;
40 ya kuma kawo bunsuru ɗaya domin hadaya don zunubi;
41 da shanu biyu, raguna biyar, bunsurai biyar da kuma ʼyan raguna biyar,
dukansu bana ɗaya-ɗaya, a miƙa su hadaya ta salama.
Wannan ita ce hadayar Shelumiyel ɗan Zurishaddai.

42 A rana ta shida, Eliyasaf ɗan Deyuwel, shugaban mutanen Gad, ya kawo
hadayarsa.
43 Hadayar da ya kawo ita ce,
faranti guda ɗaya na azurfa, nauyinsa shekel ɗari ɗaya da talatin, da kuma daro
na yayyafawa na azurfa, nauyinsa shekel sabaʼin, dukan biyu, an auna su bisa
ga maʼaunin shekel na tsattsarkan wuri, kowannensu cike da lallausan gari,
haɗe da mai kamar hadaya ta gari;
44 ya kuma kawo kwanon zinariya ɗaya mai nauyin shekel goma, cike da turaren
hayaƙi;
45 da ƙaramin bijimi guda ɗaya, tunkiya ɗaya, da rago, dukansu bana ɗaya-ɗaya
domin hadaya ta ƙonawa;
46 ya kuma kawo bunsuru ɗaya domin hadaya don zunubi;
47 da shanu biyu, raguna biyar, bunsurai biyar da kuma ʼyan raguna biyar,
dukansu bana ɗaya-ɗaya, a miƙa su hadaya ta salama.
Wannan ita ce hadayar Eliyasaf ɗan Deyuwel.

48 A rana ta bakwai, Elishama ɗan Ammihud, shugaban mutanen Efraim, ya
kawo hadayarsa.
49 Hadayar da ya kawo ita ce,
faranti guda ɗaya na azurfa, nauyinsa shekel ɗari ɗaya da talatin, da kuma daro
na yayyafawa na azurfa, nauyinsa shekel sabaʼin, dukan biyu, an auna su bisa
ga maʼaunin shekel na tsattsarkan wuri, kowannensu cike da lallausan gari,
haɗe da mai kamar hadaya ta gari;
50 kwanon zinariya ɗaya mai nauyin shekel goma, cike da turaren hayaƙi;
51 da ƙaramin bijimi guda ɗaya, tunkiya ɗaya, da rago, dukansu bana ɗaya-ɗaya
domin hadaya ta ƙonawa;
52 ya kuma kawo bunsuru ɗaya domin hadaya don zunubi;
53 da shanu biyu, raguna biyar, bunsurai biyar da kuma ʼyan raguna biyar,
dukansu bana ɗaya-ɗaya, a miƙa su hadaya ta salama.

Wannan ita ce hadayar Elishama ɗan Ammihud.

54 A rana ta takwas, Gamaliyel ɗan Fedazur, shugaban mutanen Manasse, ya kawo hadayarsa.
55 Hadayar da ya kawo ita ce,
faranti guda ɗaya na azurfa, nauyinsa shekel ɗari ɗaya da talatin, da kuma daro na yayyafawa na azurfa, nauyinsa shekel saba'in, dukan biyu, an auna su bisa ga ma'aunin shekel na tsattsarkan wuri, kowannensu cike da lallausan gari, haɗe da mai kamar hadaya ta gari;
56 kwanon zinariya ɗaya mai nauyin shekel goma, cike da turaren hayaƙi;
57 da ƙaramin bijimi guda ɗaya, tunkiya ɗaya, da rago, dukansu bana ɗaya-ɗaya domin hadaya ta ƙonawa;
58 ya kuma kawo bunsuru ɗaya domin hadaya don zunubi;
59 da shanu biyu, raguna biyar, bunsurai biyar da kuma 'yan raguna biyar, dukansu bana ɗaya-ɗaya, a miƙa su hadaya ta salama.
Wannan ita ce hadayar Gamaliyel ɗan Fedazur.

60 A rana ta tara, Abidan ɗan Gideyoni, shugaban mutanen Benyamin, ya kawo hadayarsa.
61 Hadayar da ya kawo ita ce,
faranti guda ɗaya na azurfa, nauyinsa shekel ɗari ɗaya da talatin, da kuma daro na yayyafawa na azurfa, nauyinsa shekel saba'in, dukan biyu, an auna su bisa ga ma'aunin shekel na tsattsarkan wuri, kowannensu cike da lallausan gari, haɗe da mai kamar hadaya ta gari;
62 kwanon zinariya ɗaya mai nauyin shekel goma, cike da turaren hayaƙi;
63 da ƙaramin bijimi guda ɗaya, tunkiya ɗaya, da rago, dukansu bana ɗaya-ɗaya domin hadaya ta ƙonawa;
64 ya kuma kawo bunsuru ɗaya domin hadaya don zunubi;
65 da shanu biyu, raguna biyar, bunsurai biyar da kuma 'yan raguna biyar, dukansu bana ɗaya-ɗaya, a miƙa su hadaya ta salama.
Wannan ita ce hadayar Abidan ɗan Gideyoni.

66 A rana ta goma, Ahiyezer ɗan Ammishaddai, shugaban mutanen Dan, ya kawo hadayarsa.
67 Hadayar da ya kawo ita ce,
faranti guda ɗaya na azurfa, nauyinsa shekel ɗari ɗaya da talatin, da kuma daro na yayyafawa na azurfa, nauyinsa shekel saba'in, dukan biyu, an auna su bisa ga ma'aunin shekel na tsattsarkan wuri, kowannensu cike da lallausan gari, haɗe da mai kamar hadaya ta gari;
68 kwanon zinariya ɗaya mai nauyin shekel goma, cike da turaren hayaƙi;
69 da ƙaramin bijimi guda ɗaya, tunkiya ɗaya, da rago, dukansu bana ɗaya-ɗaya domin hadaya ta ƙonawa;
70 ya kuma kawo bunsuru ɗaya domin hadaya don zunubi;
71 da shanu biyu, raguna biyar, bunsurai biyar da kuma 'yan raguna biyar, dukansu bana ɗaya-ɗaya, a miƙa su hadaya ta salama.
Wannan ita ce hadayar Ahiyezer ɗan Ammishaddai.

72 A rana ta goma sha ɗaya, Fagiyel ɗan Okran, shugaban mutanen Asher, ya kawo hadayarsa.
73 Hadayar da ya kawo ita ce,

faranti guda ɗaya na azurfa, nauyinsa shekel ɗari ɗaya da talatin, da kuma daro na yayyafawa na azurfa, nauyinsa shekel saba'in, dukan biyu, an auna su bisa ga ma'aunin shekel na tsattsarkan wuri, kowannensu cike da lallausan gari, haɗe da mai kamar hadaya ta gari;
74 kwanon zinariya ɗaya mai nauyin shekel goma, cike da turaren hayaƙi;
75 da ƙaramin bijimi guda ɗaya, tunkiya ɗaya, da rago, dukansu bana ɗaya-ɗaya domin hadaya ta ƙonawa;
76 ya kuma kawo bunsuru ɗaya domin hadaya don zunubi;
77 da shanu biyu, raguna biyar, bunsurai biyar da kuma 'yan raguna biyar, dukansu bana ɗaya-ɗaya, a miƙa su hadaya ta salama.

Wannan ita ce hadayar Fagiyel ɗan Okran.

78 A rana ta goma sha biyu, Ahira ɗan Enan, shugaban mutanen Naftali, ya kawo hadayarsa.
79 Hadayar da ya kawo ita ce,
faranti guda ɗaya na azurfa, nauyinsa shekel ɗari ɗaya da talatin, da kuma daro na yayyafawa na azurfa, nauyinsa shekel saba'in, dukan biyu, an auna su bisa ga ma'aunin shekel na tsattsarkan wuri, kowannensu cike da lallausan gari, haɗe da mai kamar hadaya ta gari;
80 kwanon zinariya ɗaya mai nauyin shekel goma, cike da turaren hayaƙi;
81 da ƙaramin bijimi guda ɗaya, tunkiya ɗaya, da rago, dukansu bana ɗaya-ɗaya domin hadaya ta ƙonawa;
82 ya kuma kawo bunsuru ɗaya domin hadaya don zunubi;
83 da shanu biyu, raguna biyar, bunsurai biyar da kuma 'yan raguna biyar, dukansu bana ɗaya-ɗaya, a miƙa su hadaya ta salama.

Wannan ita ce hadayar Ahira ɗan Enan.

84 Waɗannan su ne hadayun shugabannin Isra'ilawa saboda keɓewar bagade sa'ad da aka shafe shi,
an kawo faranta goma sha biyu na azurfa, darunan goma sha biyu na azurfa don yayyafawa, da kuma kwanonin zinariya goma sha biyu. 85 Kowane faranti
na azurfa yana da nauyin shekel ɗari da talatin, kuma kowane daro na azurfa don yayyafawa yana da nauyin shekel saba'in. Duka-duka dai, nauyin kwanonin azurfa, shekel dubu biyu ne da ɗari huɗu, bisa ga ma'aunin shekel
na tsattsarkan wuri. 86 Kwanonin zinariya goma sha biyu da aka cika da
turaren hayaƙi kuwa, nauyinsu shekel goma ne kowanne, bisa ga ma'aunin shekel na tsattsarkan wuri. Duka-duka dai, nauyin kwanonin zinariya, shekel ɗari ɗaya ne da ashirin.
87 Jimillar dabbobi don hadaya ta ƙonawa, ta kai ƙanana bijimai goma sha biyu, raguna goma sha biyu da 'yan raguna goma sha biyu, dukansu bana ɗaya-ɗaya, tare da hadayarsu ta hatsi. Aka yi amfani da bunsurai goma sha biyu domin hadaya don zunubi.
88 Jimillar dabbobi don hadaya ta salama, ta kai shanu ashirin huɗu, raguna sittin, bunsurai sittin da kuma 'yan raguna sittin, dukansu bana ɗaya-ɗaya.

Waɗannan su ne hadayu saboda keɓewar bagade, bayan an shafe shi.

89 Sa'ad da Musa ya shiga Tentin Sujada don yă yi magana da UBANGIJI, sai ya
ji murya tana magana da shi daga tsakanin kerubobi biyu a bisa murfin akwatin
Alkawari. A ta haka UBANGIJI ya yi masa magana.

# 8

### *Shiryawa fitilu*

1 Ubangiji ya ce wa Musa, 2 “Yi magana da Haruna, ka ce masa, ‘Sa’ad da za ka
shisshirya fitilun nan bakwai, ka shirya su yadda za su fuskanci gaba domin haskensu
yă haskaka ta gaba.’ ”
3 Haka kuwa Haruna ya yi; ya shisshirya fitilun yadda za su fuskanci gaba a kan
wurin ajiye fitilan, kamar dai yadda Ubangiji ya umarci Musa. 4 Ga yadda aka yi
wurin ajiye fitilan. An ƙera shi da zinariya daga gindinsa har zuwa sama inda ya
buɗu. Aka ƙera wurin ajiye fitilan yadda Ubangiji ya nuna wa Musa.

### *Keɓewar Lawiyawa*

5 Ubangiji ya ce wa Musa, 6 “Keɓe Lawiyawa daga sauran Isra’ilawa, ka tsarkake
su. 7 Ga yadda za ka tsarkake su, ka yayyafa musu ruwan tsarkakewa; ka sa su aske
jikunansu duka su kuma wanke tufafinsu, ta haka za su tsarkake kansu. 8 Ka sa su
ɗauki ɗan bijimi tare da lallausan garin hadaya, kwaɓaɓɓe da mai; sa’an nan, kai
kuma ka ɗauki ɗan bijimi na biyu na hadaya don zunubi. 9 Ka kawo Lawiyawa a
gaban Tentin Sujada, ka kuma kira taron Isra’ilawa duka. 10 Za ka kawo Lawiyawa a
gaban Ubangiji, Isra’ilawa kuma za su ɗibiya musu hannuwansu. 11 Haruna zai miƙa
Lawiyawa a gaban Ubangiji a matsayin hadaya ta kaɗawa daga Isra’ilawa, saboda a
shirya su domin aikin Ubangiji.
12 “Bayan Lawiyawa sun ɗibiya hannuwansu a kan bijiman, sai ka yi amfani da
ɗaya a matsayin hadaya don zunubi ga Ubangiji, ɗayan kuma domin hadaya ta
ƙonawa, don yin kafara saboda Lawiyawa. 13 Ka kuma sa Lawiyawa su tsaya a gaban
Haruna da ’ya’yansa, sai ka miƙa su kamar hadaya ta kaɗawa ga Ubangiji. 14 Da haka
za ka keɓe Lawiyawa daga sauran Isra’ilawa, Lawiyawa za su zama nawa.
15 “Bayan ka tsarkake Lawiyawa, ka kuma miƙa su kamar hadaya ta kaɗawa, sai su
zo su yi aikinsu a Tentin Sujada. 16 Gama dukansu an ba ni su daga cikin Isra’ilawa
a maimakon dukan waɗanda suka fara buɗe mahaifa, wato, dukan ’ya’yan farin
Isra’ilawa. Na karɓi Lawiyawa su zama nawa. 17 Kowane ɗan farin haihuwa, ko
mutum, ko dabba a Isra’ila, nawa ne. Sa’ad da na kashe ’ya’yan fari a Masar, na
keɓe ’ya’yan fari na Isra’ilawa wa kaina. 18 Na kuma ɗauki Lawiyawa a maimakon
dukan ’ya’yan fari maza a Isra’ila. 19 Cikin dukan Isra’ilawa, na ba da Lawiyawa
kyauta ga Haruna da ’ya’yansa, su yi hidima a Tentin Sujada a madadin Isra’ilawa,
su kuma yi kafara dominsu saboda kada annoba ta bugi Isra’ilawa sa’ad da suka je
kusa da wuri mai tsarki.”
20 Musa, Haruna da kuma dukan taron Isra’ilawa, suka yi da Lawiyawa yadda
Ubangiji ya umarci Musa. 21 Lawiyawa suka tsarkake kansu, suka kuma wanke
tufafinsu. Sai Haruna ya miƙa su kamar hadaya ta kaɗawa a gaban Ubangiji, ya
kuma yi kafara saboda su don yă tsarkake su. 22 Bayan haka, sai Lawiyawa suka
zo don su yi aikinsu a Tentin Sujada, a ƙarƙashin Haruna da ’ya’yansa. Suka yi da
Lawiyawa kamar dai yadda Ubangiji ya umarci Musa.
23 Ubangiji ya ce wa Musa, 24 “Wannan ya shafi Lawiyawa ne, wato, mazan da suka
kai shekara ashirin da biyar, ko fiye, za su zo su yi aiki a Tentin Sujada, 25 amma
in suka kai shekaru hamsin da haihuwa, dole su huta daga wannan aiki na yau da
kullum, su kuma daina aiki. 26 Za su iya taimakon ’yan’uwansu cikin tafiyar da
ayyuka a Tentin Sujada, amma su kansu ba za su yi aikin ba. Haka fa za ka ba wa
Lawiyawa aikinsu.”

# 9

### *Bikin Ketarewa*

1 Ubangiji ya yi magana da Musa a Hamadar Sinai, a watan farko na shekara ta
biyu bayan fitarsu daga ƙasar Masar. Ya ce, 2 “Ka sa Isra’ilawa su yi Bikin Ketarewa
a ƙayyadadden lokaci. 3 A yi wannan bikin ƙayyadadden lokaci da yamma, a rana
ta goma sha huɗu ga wannan wata, a yi shi bisa ga dokokinsa da ƙa’idodinsa.”
4 Saboda haka sai Musa ya gaya wa Isra’ilawa su yi Bikin Ketarewa, 5 suka kuwa
yi haka a Hamadar Sinai da yamma, a rana ta sha huɗu ga watan farko. Isra’ilawa
suka yi dukan abubuwa yadda Ubangiji ya umarci Musa.
6 Amma waɗansunsu ba su iya yin Bikin Ketarewa a ranar ba gama sun ƙazantu
ta wurin taɓa gawa. Saboda haka suka zo wurin Musa da Haruna a wannan rana
7 suka ce wa Musa, “Mun ƙazantu saboda mun taɓa gawa, don me aka hana mu mu
ba da hadaya ga Ubangiji tare da sauran Isra’ilawa a ƙayyadadden lokaci?”
8 Musa ya amsa musu ya ce, “Ku dakata sai na sami umarni daga wurin Ubangiji
game da ku.”
9 Sai Ubangiji ya ce wa Musa, 10 “Gaya wa Isra’ilawa cewa, ‘Sa’ad da waninku ko
zuriyarku ya ƙazantu ta wurin taɓa gawa, ko kuwa ya yi tafiya mai nisa, duk da haka
zai kiyaye Bikin Ketarewa ta Ubangiji. 11 Za su yi bikin da yamma, a rana ta sha huɗu
ga wata na biyu. Za su ci naman tunkiya, tare da burodi marar yisti, da ganyaye masu
ɗaci. 12 Kada su bar kome daga cikinsa yă kai safe, ko a karye ƙashinsa. Sa’ad da suke
Bikin Ketarewa, dole su kiyaye dukan ƙa’idodinsa. 13 Amma in mutumin da yake da
tsarki bai kuma yi tafiya ba, ya kuwa ƙi yă yi Bikin Ketarewar, dole a ware wannan
mutum daga mutanensa, domin bai miƙa hadaya ga Ubangiji a ƙayyadadden lokaci
ba. Wannan mutum zai ɗauki alhakin zunubinsa.
14 “ ‘Baƙon da yake zaune a cikinku wanda yake so yă yi Bikin Ketarewar Ubangiji,
dole yă yi shi bisa ga dokokinsa da ƙa’idodinsa. Dole ku kasance da ƙa’ida ɗaya ga
baƙo da kuma ɗan ƙasa.’ ”

### *Girgije a bisa tabanakul*
### *(Fitowa 40.34-38)*

15 A ranar da aka kafa Tenti na Alkawari, sai girgije ya rufe shi. Daga yamma har
safe, girgijen da yake bisa tabanakul ya yi kama da wuta. 16 Haka ya ci gaba da
kasancewa; girgijen ya rufe shi, da dare kuma sai ya yi kamar wuta. 17 Duk sa’ad
da aka ɗaga girgijen daga Tentin, sai Isra’ilawa su kama hanya; duk inda girgijen
ya tsaya, a nan Isra’ilawa za su yi sansani. 18 Da umarnin Ubangiji, Isra’ilawa suke
tashi. Da umarninsa kuma suke sauka. Muddin girgijen yana tsaye a bisa tabanakul,
sukan yi ta zamansu a sansanoni. 19 Sa’ad da girgijen ya ci gaba da kasancewa a
bisan tabanakul na dogon lokaci, Isra’ilawa sukan bi umarnin Ubangiji, ba kuwa za
su tashi ba. 20 Wani lokaci girgijen yakan yi ’yan kwanaki ne kawai a bisa tabanakul;
da umarnin Ubangiji sukan kafa sansani da umarninsa kuma su tashi. 21 Wani lokaci
girgijen yakan zauna daga yamma har safiya ne kawai, sa’ad da kuma aka ɗaga shi
da safe, sai su kama hanya. Ko da rana, ko da dare, duk sa’ad da aka ɗaga girgijen,
sai su ma su tashi. 22 Ko girgijen ya yi kwana biyu a bisa tabanakul, ko wata guda,
ko shekara, Isra’ilawa za su zauna a sansani ba kuwa za su tashi ba; amma sa’ad
da aka ɗaga shi, sai su kuma su tashi. 23 Da umarnin Ubangiji sukan kafa sansani,
da umarninsa kuma sukan tashi. Sukan bi umarnin Ubangiji, bisa ga umarninsa ta
wurin Musa.

# 10

### *Kakakin azurfa*

1 Ubangiji ya ce wa Musa, 2 “Ka ƙera kakaki guda biyu na azurfa, ka kuma yi amfani
da su don kira taron jama’a wuri ɗaya, don kuma ka riƙa sanar da su lokacin tashi
daga sansani. 3 Sa’ad da aka busa su biyu, dukan jama’a za su taru a gabanka a ƙofar

Tentin Sujada. 4 In ɗaya ne kaɗai aka busa, sai shugabannin kabilan Isra'ila, su taru
a gabanka. 5 Sa'ad da aka ji karar busar kakaki, sai sansanin da yake a gabashi, su
kama hanya. 6 A kara ta biyu, sansanin da yake a kudanci, su kama hanya. Busan
kakaki zai zama alama ta kama hanya. 7 In don a tara jama'a ne, sai a busa kakaki,
amma ba da irin alama ɗaya ba.
8 "'Ya'yan Haruna, firistoci ne, za su busa kakaki. Wannan za tă zama
dawwammamiyar farilla gare ku da kuma tsararraki masu zuwa. 9 Duk lokacin da
za ku tafi yaƙi a ƙasarku, in akwai waɗansu da suke matsa muku, za ku yi amfani da
waɗannan kakaki ta wurin hura su, alama ce, cewa za a je yaƙi. Sa'an nan UBANGIJI
Allahnku zai tuna da ku, yă cece ku daga maƙiyanku. 10 Haka ma in kuna cikin jin
daɗinku, musamman lokacin da kuke bukukkuwanku, kamar Bikin Sabon Wata da
dai kowane Bikinku, za ku hura waɗannan kakaki lokacin da kuke miƙa hadayunku
na ƙonawa, da hadayunku na salama, za su kuma zama muku abin tunawa a gaban
Allahnku. Ni ne UBANGIJI Allahnku."

### *Isra'ilawa sun bar Sinai*

11 A rana ta ashirin ga wata na biyu, a shekara ta biyu, sai girgijen ya tashi daga
tabanakul na Shaida. 12 Sai Isra'ilawa suka tashi daki-daki daga Hamadar Sinai, suna
tafiya daga wuri zuwa wuri, har sai da girgijen ya tsaya a Hamadar Faran. 13 Suka
kama hanya, a wannan lokaci, bisa umarnin UBANGIJI, ta wurin Musa.
14 Ɓangarorin sansanin Yahuda suka fara tashi, bisa ga ƙa'idar da aka yi, aka
kuma umarta. Nashon ɗan Amminadab ne shugaba. 15 Netanel ɗan Zuwar ne
shugaban ɓangaren kabilar Issakar, 16 Eliyab ɗan Helon kuma shi ne shugaban
ɓangaren kabilar Zebulun. 17 Sa'an nan aka saukar da tabanakul ƙasa, Gershonawa
da mutanen Merari da suke ɗauke da shi suka kama hanya.
18 Sai ɓangarori sansanin Ruben suka biyo, bisa ga ƙa'idar da aka yi, aka kuma
umarta. Elizur ɗan Shedeyur ne shugaba. 19 Shelumiyel ɗan Zurishaddai ne
shugaban ɓangaren kabilar Simeyon, 20 Eliyasaf ɗan Deyuwel kuma shi ne shugaban
ɓangaren kabilar Gad. 21 Sai Kohatawa suka kama hanya, ɗauke da kayayyaki masu
tsarki, domin kafin su kai wurin da za a kafa sansani, a riga an kafa tabanakul.
22 Biye da waɗannan kuma sai ɓangaren sansanin kabilar Efraim suka biyo bisa ga
ƙa'ida da aka yi, aka kuma umarta. Elishama ɗan Ammihud ne shugaba. 23 Gamaliyel
ɗan Fedazur ne shugaban ɓangaren kabilar Manasse, 24 Abidan ɗan Gideyoni kuma
shi ne shugaban ɓangaren kabilar Benyamin.
25 A ƙarshe, a matsayi masu gadin bayan dukan ɓangarori, sai ɓangaren sansanin
Dan suka tashi bisa ga ƙa'idar da aka yi, aka kuma umarta. Ahiyezer ɗan
Ammishaddai ne shugaba. 26 Fagiyel ɗan Okran ne shugaban ɓangaren kabilan
Asher, 27 Ahira ɗan Enan kuma shi ne shugaban kabilar Naftali. 28 Wannan shi ne
tsarin tafiyar ɓangarorin Isra'ilawa, sa'ad da sukan kama hanya.
29 Sai Musa ya ce wa Hobab ɗan Reyuwel Bamidiyane surukinsa, "Yanzu fa, muna
shirin tashi ne daga nan, domin mu tafi inda UBANGIJI ya ce, 'Zan ba ku.' Ka zo
tare da mu, za mu kuwa yi maka alheri, gama UBANGIJI ya yi wa Isra'ilawa alkawari
abubuwa masu kyau."
30 Ya amsa, ya ce "A'a, ba zan tafi ba; zan koma ƙasata da kuma wurin mutanena."
31 Amma Musa ya ce, "Ina roƙonka kada ka rabu da mu. Ka san inda ya kamata
mu kafa sansani a hamada, za ka kuma zama idanunmu. 32 In ka zo tare da mu, za
mu raba duk abin alherin UBANGIJI ya ba mu tare da kai."
33 Saboda haka suka kama hanya daga dutsen UBANGIJI, suka yi tafiya kwana uku.
Akwatin alkawarin UBANGIJI ya ja gabansu a waɗannan kwanaki uku, don yă samo
musu masauƙi. 34 A duk lokacin da suka tashi daga sansani, girgijen UBANGIJI ya
inuwantar da su da rana.

35 Duk kuma sa'ad da akwatin ya kama hanya, sai Musa ya ce,
"Ka tashi, ya UBANGIJI!
Ka sa maƙiyanka su warwatse;
masu ƙinka kuma su gudu a gabanka."
36 Duk sa'ad da akwatin ya sauka kuma, sai Musa ya ce,
"Ka komo, ya UBANGIJI,
a wurin dubban da ba a iya ƙidayawa na iyalan Isra'ila."

# 11

### *Wuta daga wurin UBANGIJI*

1 Da UBANGIJI ya ji gunagunin da mutanen suke yi saboda wahalarsu, sai ya husata
ƙwarai. Sai wuta daga UBANGIJI ta yi ta ci a cikinsu har ta ƙone waɗansu wurare na
sansanin. 2 Da jama'ar suka yi wa Musa kuka, sai ya yi addu'a ga UBANGIJI, wutar
kuwa ta mutu. 3 Saboda haka aka kira wannan wuri Tabera, gama a wurin ne wuta
daga UBANGIJI ta ƙuna a cikinsu.

### *Makware daga UBANGIJI*

4 Wata rana, baƙin da suke cikinsu, suka fara kwaɗayin waɗansu abinci, har suka
sa Isra'ilawa suka fara kuka, suna cewa, "Da mun sami nama mun ci mana! 5 Mun
tuna da kifin da muka ci kyauta a Masar, haka ma kayan lambu irin su kukumba,
guna, safa, albasa da kuma tafarnuwa. 6 Amma ga shi yanzu ba mu da wani abin
marmari; in ba wannan Manna ba!"
7 Manna kuwa kamar tsabar riɗi take, kamanninta kuma kamar ƙaro ne. 8 Mutane
sukan fita su tattara ta, su niƙa a dutsen niƙa, ko kuwa su daka a turmi. Su dafa,
ko su yi waina da ita. Ɗanɗanonta yakan yi kamar abin da aka yi da man zaitun.
9 Sa'ad da raɓa tana saukowa da dad dare a kan sansani, Manna ma takan sauko.
10 Musa ya ji mutanen suna ta gunaguni ko'ina a cikin iyalansu, kowane mutum
a ƙofar tentinsa. UBANGIJI kuwa ya husata ƙwarai, sai Musa ya damu. 11 Sai ya ce
wa UBANGIJI, "Me ya sa ka kawo wannan damuwar a kan bawanka? Me na yi da ya
ɓata maka rai har ka ɗora dukan nauyin mutanen nan a kaina? 12 Ni ne na yi cikin
dukan mutanen nan? Ni ne na haife su? To, me ya sa ka ce in ɗauke su a ƙirjina
kamar yadda mai reno yake rungume jariri, zuwa ƙasa wadda ka yi alkawari da
rantsuwa za ka ba wa kakanninsu? 13 Ina ne zan sami nama in waɗannan mutane?
Sun dinga yin mini kuka suna cewa 'Ka ba mu nama mu ci!' 14 Ba zan iya ɗaukan
dukan mutanen nan ni kaɗai ba, nauyin ya yi mini yawa. 15 In haka za ka yi da ni,
ka kashe ni yanzu, in na sami tagomashi daga gare ka, kada ka bar ni in rayu in ga
wannan baƙin ciki."
16 Sai UBANGIJI ya ce wa Musa, "Ka tattaro mini dattawa saba'in daga cikin mutanen
Isra'ila, waɗanda aka sani su ne dattawa da kuma shugabanni a cikin jama'a. Ka sa
su zo Tentin Sujada, su tsaya a can tare da kai. 17 Zan sauko in yi magana da kai a
can, zan kuma ɗauki Ruhun da yake kanka in mai da shi wajensu. Za su taimake ka
ɗaukan nauyin mutane, don yă zama ba kai kaɗai ba ne mai ɗaukan kaya.
18 "Ka gaya wa mutane, 'Ku tsarkake kanku don gobe, za ku ci nama. UBANGIJI ya
ji ku sa'ad da kuka yi kuka cewa, "Da mun sami nama mun ci mana! Ai, da ba mu
da damuwa, gama lokacin da muke zama cikin Masar ba mu da damuwa!" Yanzu
UBANGIJI zai ba ku nama, za ku kuma ci. 19 Ba za ku ci shi na kwana ɗaya, ko biyu,
ko biyar, ko goma, ko kuma kwana ashirin kaɗai ba, 20 amma za ku ci har na wata
guda cur, sai ya gundure ku a hanci har ku yi ƙyamarsa, domin kun ƙi UBANGIJI
wanda yake cikinku, kuka yi kuka a gabansa, kuna cewa, "Don me ma muka bar
ƙasar Masar?" ' "

21 Amma Musa ya ce, “Ga ni a cikin mutane dubu ɗari shida tafe tare da ni, kana
kuma cewa, ‘Zan ba su nama su ci har wata guda cur!’ 22 Za su ma sami isashe in
har aka yanka musu garkuna tumaki da na shanu? Za su sami isashe in aka kama
musu dukan kifin teku?”
23 Ubangiji ya ce wa Musa, “Akwai abin da ya fi ƙarfina ne? Bari ka gani ko abin
da na ce zan yi, zai faru ko babu.”
24 Saboda haka Musa ya fita ya gaya wa jama’a abin da Ubangiji ya faɗa. Ya tattaro
dattawansu saba’in, ya sa suka tsaya kewaye da Tentin Sujada.
25 Sa’an nan Ubangiji ya sauko daga girgije, ya yi magana da shi, ya kuma ɗauke
Ruhun da yake kan Musa ya ɗora shi a kan dattawa saba’in nan. Sa’ad da Ruhun ya
zauna a kansu, sai suka yi annabci, amma daga wannan ba su ƙara yin haka kuma
ba.
26 To, fa, akwai dattawa biyu da suka kasance a sansani, wato, Eldad da Medad.
Su ma an lasafta su cikin dattawan, amma ba su fita zuwa Tentin Sujada ba. Duk
da haka Ruhun ya sauka a kansu, suka kuma yi annabci a cikin sansanin. 27 Wani
saurayi ya sheƙa a guje zuwa wajen Musa ya ce, “Eldad da Medad suna can suna
annabci a sansani.”
28 Sai Yoshuwa ɗan Nun, wanda yake mataimakin Musa tun yana saurayi, ya amsa
ya ce, “Ranka yǎ daɗe, Musa, ka hana su!”
29 Amma Musa ya amsa ya ce, “Kana kishi domina ne? Da ma a ce dukan mutanen
Ubangiji annabawa ne, da ma a kuma ce Ubangiji ya sa Ruhunsa a kansu mana!”
30 Sai Musa da dattawan Isra’ila suka koma sansani.
31 Ana nan, sai Ubangiji ya kawo wata iska mai tsanani ta koro makware daga
teku. Ta bar su birjik kewaye da sansani, tsayinsu daga ƙasa ya kai kamu biyu,
misalin tafiyar nisan yini guda ta kowace fuska. 32 Dukan yini da dukan dare da
kuma kashegari, mutane suka fito suka tattara makware. Ba wanda ya kāsa tara
ƙasa da garwa goma. Sai suka shanya abinsu kewaye da sansanin. 33 Amma da
suna cikin cin naman, tun ba su ma haɗiye ba, sai Ubangiji ya husata sosai a kan
jama’ar, ya buge su da annoba mai zafi. 34 Saboda haka aka kira wannan wuri Kibrot
Hatta’awa,* gama a can ne aka binne mutanen nan makwaɗaita.
35 Daga Kibrot Hatta’awa, mutane suka yi tafiya zuwa Hazerot, a can suka sauka.

# 12

*Miriyam da Haruna sun tayar wa Musa*

1 Miriyam da Haruna suka fara zargin Musa saboda matarsa ’yar ƙasar Kush da
ya aura. 2 Suka ce, “Ubangiji ya yi magana ta wurin Musa ne kaɗai? Ashe, bai yi
magana ta wurinmu mu ma ba?” Ubangiji kuwa ya ji wannan.
3 (Musa kuwa mutum ne mai tawali’u ƙwarai, mafi tawali’u fiye da kowane mutum
a duniya.)
4 Nan da nan Ubangiji ya ce wa Musa, da Haruna da kuma Miriyam, “Ku fita ku
tafi Tentin Sujada, dukanku uku.” Sai dukansu uku suka tafi. 5 Sai Ubangiji ya sauko
a cikin ginshiƙin girgije; ya tsaya a bakin ƙofar Tenti, ya kira Haruna da Miriyam.
Sa’ad da su biyu suka gusa gaba, 6 sai ya ce, “Ku ji abin da zan faɗa,
“Duk lokacin da akwai annabin Ubangiji a cikinku,
nakan bayyana kaina gare shi cikin wahayi,
in yi magana da shi cikin mafarkai.
7 Amma ba haka nake magana da Musa bawana ba;
na sa shi yǎ lura da dukan jama’ata Isra’ila.
8 Da shi nake magana fuska da fuska,

---

* **11:34** Kibrot Hatta’awa yana nufin makabartan kwaɗayi.

a fili kuma, ba a kacici-kacici ba;
yakan ga siffar UBANGIJI.
To, me ya sa ba ku ji tsoro
ku yi magana a kan bawana Musa ba?"
9 Sai fushin UBANGIJI ya yi ƙuna a kansu, ya kuma rabu da su.
10 Da girgijen ya tashi daga bisa Tentin, sai ga Miriyam tsaye, kuturwa, fari fat.
Haruna kuwa ya juya wajenta ya ga ta kuturce; 11 sai Haruna ya ce wa Musa, "Ranka
yă daɗe, ina roƙonka kada ka hukunta mu, gama zunubin da muka yi, mun yi ne cikin
wauta. 12 Kada ka sa ta zama kamar haifaffen mataccen jariri daga cikin mahaifiya
wanda rabin jikin ruɓaɓɓe ne."
13 Saboda haka sai Musa ya yi kuka ga UBANGIJI ya ce, "Ya Allah, ina roƙonka ka
warkar da ita!"
14 Sai UBANGIJI ya ce wa Musa, "Da a ce mahaifinta ne ya tofa mata miyau a fuskarta,
ashe, ba za tă ji kunya har kwana bakwai ba? A fitar da ita bayan sansani kwana
bakwai; bayan haka za a iya dawo da ita." 15 Haka aka fitar da Miriyam bayan sansani
kwana bakwai, mutane kuwa ba su ci gaba da tafiya ba sai da aka dawo da ita.
16 Bayan haka sai mutane suka bar Hazerot suka sauka a Hamadan Faran.

# 13

*Leƙen asirin ƙasar Kan'ana*
*(Maimaitawar Shari'a 1.19-33)*

1 UBANGIJI ya ce wa Musa, 2 "Ka aiki waɗansu mutane zuwa ƙasar Kan'ana, wadda
nake ba Isra'ilawa. Daga kowace kabila, ka aiki ɗaya daga cikin shugabanninta."
3 Saboda haka bisa ga umarnin UBANGIJI, Musa ya aike su daga Hamadan Faran.
Dukansu kuwa shugabanni ne na Isra'ilawa.

4 Shugabannin kuwa su ne,

Shammuwa ɗan Zakkur, daga kabilar Ruben;
5 Shafat ɗan Hori, daga kabilar Simeyon;
6 Kaleb ɗan Yefunne, daga kabilar Yahuda;
7 Igal ɗan Yusuf, daga kabilar Issakar;
8 Hosheya ɗan Nun, daga kabilar Efraim;
9 daga kabilar Benyamin, Falti ɗan Rafu;
10 Gaddiyel ɗan Sodi, daga kabilar Zebulun;
11 Gaddi ɗan Susi, daga kabilar Manasse (wata kabilar Yusuf);
12 Ammiyel ɗan Gemalli, daga kabilar Dan;
13 Setur ɗan Mika'ilu, daga kabilar Asher;
14 Nabi ɗan Bofsi, daga kabilar Naftali;
15 Geyuwel ɗan Maki, daga kabilar Gad.

16 Waɗannan su ne sunayen mutanen da Musa ya aika su binciki ƙasar. (Sai
Musa ya ba Hosheya ɗan Nun, suna Yoshuwa.)

17 Sa'ad da Musa ya aike su domin su binciki Kan'ana ya ce, "Ku haura, ku ratsa ta
Negeb har zuwa ƙasar tudu. 18 Ku ga yadda ƙasar take, ku ga ko mutanen da suke
zama a can ƙarfafa ne, ko raunannu, ko su kima ne, ko kuma suna da yawa. 19 Wace
irin ƙasa ce suke zama a ciki, Mai kyau ce, ko mummuna? Waɗanne irin birane ne
suke zama a ciki? Suna da katanga, ko babu? 20 Yaya ƙasar take? Tana da wadata,

ko babu? Akwai itatuwa, ko babu? Ku yi iya ƙoƙarinku ku ɗebo daga cikin albarkar ƙasar ku kawo." (Lokacin farkon nunan inabi ne.)
21 Saboda haka suka haura, suka binciki ƙasar daga Hamadan Zin har zuwa Rehob,
wajen Lebo* Hamat. 22 Suka kuma haura ta Negeb, suka iso Hebron, inda Ahiman,
da Sheshai, da Talmai, zuriyar Anak, suke zama. (An gina Hebron da shekara bakwai
kafin a gina Zowan a Masar.) 23 Da suka iso Kwarin Eshkol,† sai suka yanko reshe
guda na nonon inabi tare da 'ya'yansa cunkus. Mutum biyu suka ɗauka shi rataye a
sanda a kafaɗarsu, suka haɗa tare da rumman da kuma ɓaure. 24 Sai aka kira wurin
Kwarin Eshkol saboda nonon inabin da suka yi cunkus, wanda Isra'ilawa suka yanko
a wurin. 25 A ƙarshen kwana arba'in sai suka komo daga bincikensu.

### *Rahoto a kan binciken*

26 Suka dawo wurin Musa, da Haruna, da dukan jama'ar Isra'ilawa, a Kadesh, a
Hamadan Faran. A can suka ba da rahoton ga dukan taron da yake wurin, suka
kuma nuna musu amfanin ƙasar. 27 Suka ce wa Musa, "Mun je ƙasar da ka aike mu,
ƙasar tana zub da madara da zuma! Ga kuma amfaninta. 28 Amma fa mazaunan can
ɗin ƙarfafa ne, an kuma kewaye biranen da manya-manyan katanga. Mun kuma ga
zuriyar Anak a can. 29 Amalekawa suna zama a Negeb; Hittiyawa, Yebusiyawa da
kuma Amoriyawa, suna zama ne a ƙasar tudu. Kan'aniyawa kuma suna zama kusa
da teku da kuma a bakin Urdun."
30 Sai Kaleb ya sa mutane suka yi shiru a gaban Musa, sai ya ce, "Ya kamata mu
tafi mu mallaki ƙasar, gama lalle za mu iya cinta."
31 Amma sauran mutanen da suka je tare da shi, suka ce, "Ba za mu iya kara da
mutanen nan ba; sun fi mu ƙarfi." 32 Sai suka yaɗa labari marar kyau ga Isra'ilawa
game da ƙasar da suka binciko. Suka ce, "Kasar da muka ratsa cikinta domin mu leƙi
asirinta, tana cinye waɗanda suke zama a cikinta. Dukan mutanen da muka gani a
wurin, ƙatti ne. 33 Mun ga Nefilimawa a can (zuriyar Anak sun fito ne daga Nefilim).
Sai muka ga kanmu kamar fāra ne kawai, haka kuwa muke a gare su."

## 14

### *Mutane sun yi tawaye*

1 A daren nan, sai dukan jama'ar suka tā da murya, suka yi kuka da ƙarfi. 2 Dukan
Isra'ilawa suka yi gunaguni a kan Musa da Haruna, dukan taron kuwa suka ce musu,
"Da ma mun mutu a Masar! Ko kuma a wannan hamada ma! 3 Don me UBANGIJI
yana kawo mu wannan ƙasa yă bar mu kawai mu mutu da takobi? A kuma kwashe
matanmu da 'ya'yanmu ganima. Ashe, bai fi mana mu koma Masar ba?" 4 Sai suka
ce wa junansu, "Mu naɗa wa kanmu shugaba, mu koma Masar."
5 Sai Musa da Haruna suka fāɗi rubda ciki a gaban jama'ar Isra'ilawa da suka taru
a can. 6 Yoshuwa ɗan Nun da Kaleb ɗan Yefunne waɗanda suke tare da masu leƙo
asirin ƙasar, suka yayyage tufafinsu 7 suka ce wa dukan taron Isra'ilawa, "Kasar da
muka ratsa, muka kuma leƙi asirinta, tana da kyau sosai. 8 In UBANGIJI ya ji daɗinmu,
zai kai mu ƙasan nan, ƙasar da take zub da madara da zuma, yă kuwa ba mu ita.
9 Sai dai kada ku tayar wa UBANGIJI. Kada kuma ku ji tsoron mutane ƙasar, domin za
mu gama da su. Kāriyarsu ta gama, amma UBANGIJI yana nan tare da mu. Kada ku
ji tsoronsu."
10 Amma taron jama'a suka ce za su jajjefe su da duwatsu. Sai ɗaukakar UBANGIJI
ta bayyana a Tentin Sujada ga dukan Isra'ilawa. 11 UBANGIJI ya ce wa Musa, "Har
yaushe mutanen nan za su rena ni? Har yaushe za su ƙi gaskata da ni, duk da yawan

* **13:21** Ko kuwa wajen ƙofar zuwa † **13:23** Eshkol yana nufin cunkus; haka ma a aya 24.

mu'ujizan da nake yi a cikinsu? 12 Zan buge su duka da annoba, in hallaka su, amma
zan mai da kai al'umma mai girma, da kuma ƙarfi fiye da su."

13 Sai Musa ya ce wa Ubangiji, "Ai, Masarawa za su ji game da wannan! Da ikonka
ka fitar da mutanen nan daga cikinsu. 14 Za su kuwa gaya wa mutanen wannan ƙasa.
Sun riga sun ji cewa kai, ya Ubangiji, kana tare da waɗannan mutane, kuma cewa
kai, ya Ubangiji, an gan ka fuska da fuska, cewa girgijenka ya tsaya bisansu, cewa
kana tafiya a gabansu cikin ginshiƙin girgije da rana, da ginshiƙin wuta kuma da
dare. 15 In ka kashe dukan mutanen nan gaba ɗaya, al'ummai da suka ji wannan
labari game da kai za su ce, 16 'Ubangiji ya kāsa kai waɗannan mutane a ƙasar da
ya yi alkawari da rantsuwa ne, shi ya sa ya kashe su a hamada.'

17 "Yanzu bari Ubangiji yǎ nuna ikonsa, kamar dai yadda ka furta. 18 'Ubangiji mai
jinkiri fushi ne, mai yawan ƙauna, mai gafarta zunubi da tawaye. Duk da haka ba ya
ƙyale mai laifi, babu horo. Yana horin 'ya'ya saboda zunubin iyayensu har tsara ta
uku, da ta huɗu.' 19 Bisa ga ƙaunarka mai girma, ka gafarta zunubin mutanen nan,
kamar dai yadda ka gafarta musu daga lokacin da suka bar Masar har zuwa yanzu."

20 Ubangiji ya amsa ya ce, "Na gafarta musu, yadda ka roƙa. 21 Duk da haka,
muddin ina raye, kuma muddin ɗaukakar Ubangiji ta cika dukan duniya, 22 ko ɗaya
daga cikinsu da suka ga ɗaukakata da mu'ujizai da na yi a Masar, da kuma a cikin
hamada, da suka ƙi yin mini biyayya, suka kuma gwada ni har sau goma, 23 ba ko
ɗayansu da zai gan ƙasar da na yi alkawari da rantsuwa zan ba wa kakanninsu.
Ba ko ɗaya da ya rena ni, da zai taɓa ganinta. 24 Amma domin Kaleb bawana ya
kasance da ruhu dabam, ya kuma bi ni da zuciya ɗaya, zan kai shi cikin ƙasar da ya
je, zuriyarsa kuwa za su gāje ta. 25 Da yake Amalekawa da Kan'aniyawa suna zama
a kwarin, gobe sai ka koma baya, ka nufi wajen hamada ta hanyar Jan Teku."*

26 Ubangiji ya ce wa Musa da Haruna, 27 "Har yaushe wannan muguwar al'umma
za tǎ yi gunaguni a kaina? Na ji koke-koken waɗannan Isra'ilawa masu gunaguni.
28 Saboda haka ka gaya musu cewa, 'Muddin ina raye, in ji Ubangiji, zan yi muku
daidai da abin da na ji kuke faɗa. 29 A cikin wannan hamadan, jikunanku za su fāɗi,
kowanne a cikinku mai shekara ashirin ko fiye, wanda aka ƙirga shi cikin ƙidaya,
wanda kuma ya yi gunaguni a kaina, da zai shiga wannan ƙasa. 30 Ba ko ɗaya daga
cikinku da zai shiga ƙasar da na ɗaga hannu na rantse, za tǎ zama gidanku, sai dai
Kaleb ɗan Yefunne da Yoshuwa ɗan Nun. 31 Amma game da 'ya'yanku da kuka ce za a
kwashe ganima, zan kawo su cikin ƙasar, su ji daɗin ƙasar wadda kuka ƙi. 32 Amma
ku, jikunanku za su fāɗi a wannan hamada. 33 'Ya'yanku za su zama makiyaya a
nan, shekaru arba'in suna shan wahala domin rashin amincinku, har sai mutum na
ƙarshe a cikinku ya kwanta a hamada. 34 Shekaru arba'in, shekara ɗaya a madadi
kwana ɗaya cikin kwanakin arba'in da kuka ɗauka kuka leƙi asirin ƙasa, za ku sha
wahala saboda zunubanku, ku kuma san abin da ake nufi da sa ni in yi gāba da ku.'
35 Ni, Ubangiji na faɗa, zan kuwa aikata waɗannan abubuwa a kan dukan muguwar
jama'an nan da suka haɗa kai, suka tayar mini. Za su sadu da ƙarshensu a wannan
hamada; a nan za su mutu."

36 Saboda haka mutanen da Musa ya aika, su leƙo asirin ƙasar, waɗanda suka
komo, suka sa taron jama'a su yi gunaguni a kansa saboda sun kawo rahoto mai
banrazana a kan ƙasar, 37 waɗannan mutanen da suka kawo rahoto mai banrazana
a kan ƙasar, annoba ta buge su, suka kuwa mutu a gaban Ubangiji. 38 Daga cikin
mutanen da suka leƙo asirin ƙasar, Yoshuwa ɗan Nun, da Kaleb ɗan Yefunne ne,
kaɗai suka rayu.

*(Maimaitawar Shari'a 1.41-45)*

* **14:25** Da Ibraniyanci Yam Suf; wato, Tekun Iwa.

39 Da Musa ya gaya wa dukan Isra'ilawa wannan labari, sai suka yi baƙin ciki
ƙwarai. 40 Kashegari da sassafe suka haura ta wajen ƙasa mai tudu suka ce, "Mun yi
zunubi, za mu tafi inda UBANGIJI ya yi alkawari."
41 Amma Musa ya ce, "Don me kuke rashin biyayya da umarnin UBANGIJI? Wannan
ba zai yiwu ba! 42 Kada ku haura, domin UBANGIJI, ba ya tare da ku. Magabtanku za
su ci nasara a kanku, 43 gama Amalekawa da Kan'aniyawa za su kara da ku a can.
Domin kun juya daga UBANGIJI, ba zai kasance da ku ba, za a kuma karkashe ku da
takobi."
44 Duk da haka, suka yi tsammani ba zai zama haka ba, sai suka haura ta wajen
ƙasa mai tudu, Musa da akwatin alkawarin UBANGIJI dai ba su gusa daga sansanin ba.
45 Sai Amalekawa da Kan'aniyawa mazaunan ƙasar tudu, suka gangaro suka auka
musu, suka bubbuge su suka kokkore su har Horma.

# 15

*Karin hadayu*

1 UBANGIJI ya ce wa Musa, 2 "Ka yi magana da Isra'ilawa, ka ce musu, 'Bayan kun
shiga ƙasar da nake ba ku a matsayin gida, 3 kuka yi hadayar da akan yi da wuta ga
UBANGIJI, daga cikin shanu, ko tumaki, abin ƙanshi mai daɗi ga UBANGIJI, ko hadaya
ta ƙonawa, ko hadayu don alkawura na musamman, ko hadayar yardar rai, ko kuma
hadaya ta biki, 4 sai shi wanda ya kawo hadayar yă miƙa wa UBANGIJI hadaya ta gari
mai laushi mai kyau, kashi ɗaya bisa goma na efa wanda aka kwaɓa da kwalaba
ɗaya na mai. 5 Da kowane ɗan rago don hadaya ta ƙonawa, a shirya kwalaba ɗaya
na ruwan inabi, a matsayin hadaya ta sha.
6 " 'In da rago ne za a miƙa, to, sai a shirya hadaya ta gari mai laushi, garin yă
zama kashi biyu bisa goma na efa. A kwaɓa shi da kashi ɗaya bisa uku na garwan
mai, 7 da kashi ɗaya bisa uku na garwan ruwan inabi, a matsayin hadaya ta sha. A
miƙa ta abin ƙanshi mai daɗi ga UBANGIJI.
8 " 'Sa'ad da kuka shirya rago don hadaya ta ƙonawa saboda alkawari na
musamman, ko hadaya ta salama ga UBANGIJI, 9 sai ku kawo hadaya ta gari tare da
bijimi, kashi ɗaya bisa uku na gari mai laushi kwaɓaɓɓe da rabin garwan mai. 10 A
kuma kawo rabin garwan ruwan inabi na hadaya ta sha. Za tă zama hadayar da aka
yi da wuta mai daɗin ƙanshi ga UBANGIJI. 11 Haka za a yi da kowane bijimi, ko rago,
ko ɗan rago, ko bunsuru. 12 Haka za a yi da kowannensu bisa ga abin da aka shirya.
13 " 'Duk wanda yake ɗan ƙasa, ta haka ne dole zai aikata waɗannan abubuwa
sa'ad da ya kawo hadaya da akan yi da wuta mai daɗin ƙanshi ga UBANGIJI. 14 Idan
baƙon da yake baƙunci a cikinku, ko kowane ne da yake tare da ku a dukan
zamananku, yana so yă ba da hadayar da akan yi da wuta don a yi ƙanshi mai
daɗi ga UBANGIJI, dole yă yi kamar yadda kuke yi. 15 Ka'ida ɗaya ce ga jama'a da
kuma baƙin da suke zama a cikinku, wannan za tă zama dawwammamiyar farilla
a dukan tsararraki masu zuwa. Da ku, da baƙi, za ku zama ɗaya a gaban UBANGIJI.
16 Doka ɗaya da ƙa'ida ɗaya za a yi aiki da ita a kan ku da kuma baƙin da suke zama
a cikinku.' "
17 UBANGIJI ya ce wa Musa, 18 "Ka yi magana da Isra'ilawa, ka ce musu, 'Sa'ad da
kuka shiga ƙasar da ina kai ku, 19 kuka ci abincin ƙasar, ku miƙa wani sashe na
amfanin ƙasar a matsayin hadaya ga UBANGIJI. 20 Ku kawo waina daga nunan fari
na ɓarzajjen hatsinku, ku kuma miƙa shi a matsayin hadaya daga masussuka. 21 A
duk tsararraki masu zuwa, za ku miƙa wannan hadaya daga nunan fari na ɓarzajjen
hatsinku ga UBANGIJI.

*Hadayu domin zunubai da ba na ganganci ba*

[22] " 'To, in ku a matsayin jama'a, da gangan kuka ƙi kiyaye waɗannan ƙa'idodi da
UBANGIJI ya ba wa Musa ba, [23] ko wani daga cikin umarnan da UBANGIJI ya ba ku ta
wurinsa, daga ranar da UBANGIJI ya ba da su, har zuwa tsararraki masu zuwa, [24] in
kuwa aka yi haka ba da gangan ba, kuma da rashin sani, sai duk jama'a su miƙa ɗan
bijimi don hadaya ta ƙonawa mai daɗin ƙanshi ga UBANGIJI, tare da ƙayyadadden
hadaya ta gari, da hadaya ta sha, da kuma bunsuru na hadaya don zunubi. [25] Firist
kuwa zai yi kafara domin dukan jama'ar Isra'ilawa, za a kuma gafarta musu, gama
ba da gangan ba ne suka aikata, kuma sun kawo wa UBANGIJI hadayar da akan yi da
wuta da kuma hadaya don zunubi saboda laifinsu. [26] Za a gafarta wa dukan jama'ar
Isra'ilawa, da baƙin da suke zama a cikinsu, gama duk laifin da aka yi da rashin sani,
yakan shafi dukan mutane.
[27] " 'Amma in mutum ɗaya ne kaɗai ya yi laifi ba da gangan ba, dole yă kawo akuya
domin hadaya don zunubi. [28] Firist zai yi kafara a gaban UBANGIJI saboda mutumin
nan da ya aikata laifi ba da gangan ba, in kuwa an yi kafara saboda shi, za a gafarta
masa. [29] Ka'ida dai za tă zama ɗaya ga duk wanda ya yi laifi ba da gangan ba, ko shi
ɗan ƙasa ne, ko kuma baƙon da yake zama a cikinku.
[30] " 'Amma duk wanda ya yi zunubi da gangan, ko shi ɗan ƙasa ne, ko baƙo,
ya saɓi UBANGIJI, dole a ware wannan mutum daga mutanensa, [31] gama ya rena
maganar UBANGIJI, ya kuma karya umarninsa. Tabbatacce za a kashe wannan
mutum, alhakinsa laifinsa kuwa yana wuyansa.' "

*An kashe mai karya ranar Asabbaci*

[32] Yayinda Isra'ilawa suke ciki hamada, sai aka sami wani mutum yana tattara itace
a ranar Asabbaci. [33] Waɗanda suka gan shi, suka kawo shi wurin Musa da Haruna
da dukan taro, [34] sai suka sa shi a gidan waƙafi don ba su riga sun san abin da za a
yi da shi ba tukuna. [35] Sai UBANGIJI ya ce wa Musa, "Dole mutumin yă mutu. Dole
dukan taron su jajjefe shi a bayan sansani." [36] Saboda haka taron suka ɗauke shi
zuwa bayan sansani, suka kuma jajjefe shi har ya mutu, yadda UBANGIJI ya umarci
Musa.

*Tuntaye a riguna*

[37] UBANGIJI ya ce wa Musa, [38] "Ka yi magana da Isra'ilawa, ka ce musu, 'A dukan
tsararraki masu zuwa, za ku sa tuntaye a gefen rigunarku, su sa zare mai ruwan
shuɗi a bisan kowane tuntu. [39] Tuntayen za su zama muku abin dubawa don ku riƙa
tunawa da dukan umarnan UBANGIJI, don kada ku bi son zuciyarku, da sha'awar
idanunku yadda kuka taɓa yi. [40] Sa'an nan za ku riƙa tuna, ku kuma aikata dukan
umarnaina ku zama tsarkaka ga Allahnku. [41] Ni ne UBANGIJI Allahnku, da ya fitar da
ku daga Masar, don in zama Allahnku. Ni ne UBANGIJI Allahnku.' "

# 16

*Kora, Datan da Abiram*

[1] Kora ɗan Izhar, wanda yake Balawe ne daga dangin Kohatawa, wata rana ya nemi
Datan da Abiram 'ya'yan Eliyab, da On ɗan Felet dukansu daga kabilar Ruben, suka
haɗa kai* [2] suka tayar wa Musa. Sai suka nemi goyon bayan sanannun shugabannin
Isra'ilawa da aka naɗa a majalisa su guda 250, [3] tare kuwa suka zo wurin Musa da
Haruna, suka ce musu, "Kun wuce gona da iri! Dukan jama'an nan masu tsarki ne,
kowannensu, UBANGIJI kuma yana tare da su. Me ya sa kuke ɗaukan kanku fiye da
taron jama'ar UBANGIJI?"
[4] Da Musa ya ji haka, sai ya fāɗi rubda ciki ya yi addu'a [5] Sai ya ce wa Kora da
dukan waɗannan da suke tare shi, "Da safe, UBANGIJI zai nuna wane ne yake nasa,

* **16:1** Ko kuwa Felet, ɗauki mutane

da kuma wane ne yake da tsarki. Zai kuma sa mutumin yă zo kusa da shi. Mutumin
da ya zaɓa kuwa zai sa yă zo kusa da shi. 6 Kai Kora da ƙungiyarka, gobe, za ku ɗauki
farantai, 7 ku zuba wuta a ciki, ku kuma zuba musu turaren wuta a gaban Ubangiji.
Sa'an nan wanda Ubangiji ya zaɓa a tsakaninmu sh ne mai tsarki. Ku Lawiyawa ku
ne kuka wuce gona da iri!"

8 Musa ya kuma ce wa Kora, "Yanzu ku saurara, ku Lawiyawa! 9 Ashe, bai ishe ku
ba, cewa Allah na Isra'ila, ya keɓe ku daga sauran jama'ar Isra'ilawa, ya kuma kawo
ku kusa da shi don ku yi aiki a tabanakul na Ubangiji, ku kuma tsaya a gaba jama'a
don ku yi musu aiki? 10 Ya kawo ku da kuma dukan 'yan'uwanku Lawiyawa kusa da
shi, amma yanzu kuna ƙoƙari ku karɓi aikin firist. 11 Kai da ƙungiyarka kun haɗa
kai kuna yi wa Haruna gunaguni, amma wane ne Haruna? A zahiri tawaye ne kuke
wa Ubangiji."

12 Sai Musa ya aika a kira Datan da Abiram, 'ya'yan Eliyab maza, amma suka ce,
"Ba za mu zo ba! 13 Bai isa ba ne da ka fitar da mu daga ƙasar mai zub da madara
da zuma, ka kawo mu nan hamada don ka kashe mu? Yanzu kuma so kake ka mai
da kanka sarki a bisanmu? 14 Ban da haka ma, ai, ba ka riga ka kai mu ƙasar mai
zub da madara da zuma ba, ba ka ba mu gādon filaye da gonakin annabi ba, yanzu
kuma kana so ka ruɗe mu. Mun ƙi, ba za mun zo ba!"

15 Sai Musa ya husata ƙwarai, ya ce wa Ubangiji, "Kada ka karɓi hadayarsu. Ban
ƙwace wani jakinsu ba, ban kuwa cuce waninsu ba."

16 Musa ya ce wa Kora, "Da kai da kuma dukan ƙungiyarka za ku bayyana a gaban
Ubangiji gobe, kai da su. Haruna ma zai kasance a can. 17 Kowannenku zai ɗauki
faranti yă zuba turare a ciki. Wato, farantai 250 ke nan, a kuma miƙa su a gaban
Ubangiji. Kai da Haruna za ku miƙa farantanku, ku ma." 18 Sai kowane mutum ya
ɗauki farantinsa, ya sa wuta da kuma turare a ciki, suka tsaya da Musa da Haruna
a ƙofar Tentin Sujada. 19 Sa'ad da Kora ya tara mabiyansa don su yi hamayya da
Musa da Haruna a ƙofar Tentin Sujada, sai ɗaukakar Ubangiji ta bayyana ga dukan
taron. 20 Ubangiji ya ce wa Musa da Haruna, 21 "Ku ware kanku daga taron nan don
in gama da su nan take."

22 Amma Musa da Haruna suka fāɗi rubda ciki suka tā da murya suka ce, "Ya Allah,
Allahn ruhohin dukan 'yan adam, za ka husata da dukan taron ne, bayan mutum
ɗaya ne ya yi zunubi?"

23 Sai Ubangiji ya ce wa Musa, 24 "Faɗa wa taron cewa, 'Ku nisanci tentin Kora, da
na Datan, da na Abiram.' "

25 Musa ya tashi ya tafi wurin Datan da Abiram, dattawan Isra'ilawa kuwa suka bi
shi. 26 Ya gargaɗe taron ya ce, "Ku ƙaurace wa tentin waɗannan mugayen mutane!
Kada ku taɓa kome da yake nasu, domin kada a shafe ku saboda zunubansu." 27 Sai
suka tashi daga inda tentin Kora, da Datan, da Abiram suke. Datan da Abiram
kuwa suka fita suna tsaye tare da matansu da 'ya'yansu da 'yan ƙanánansu a ƙofar
tentinsu.

28 Sai Musa ya ce musu, "Da haka za ku san cewa Ubangiji ne ya aiko ni, in yi
dukan waɗannan abubuwa, ba da nufin kaina na yi su ba. 29 In waɗannan mutane
sun mutu kamar yadda mutane suke mutuwa, in abin da yakan sami kowa shi ne ya
same su, to, ba Ubangiji ne ya aiko ni ba. 30 Amma in Ubangiji ya kawo wani abu
sabo, ya sa ƙasa ta buɗe bakinta, ta haɗiye su da dukan abin da suke da shi, suka
gangara cikin kabari a raye, ta haka za ku sani mutanen nan sun rena Ubangiji."

31 Nan da nan da ya gama faɗi wannan, sai ƙasa ta tsage inda Datan da Abiram
suke tsaye, 32 ta kuma buɗe bakinta, ta haɗiye su tare da mutanen gidansu da dukan
mutanen Kora da dukan abin da yake mallakarsu. 33 Suka gangara cikin kabari da
rai, tare dukan mallakarsu; ƙasa ta rufe su, suka hallaka, suka rabu da jama'ar. 34 Da

jin kukansu, dukan Isra'ilawa da suke kewaye da su suka gudu, suna ihu, “Kasa za
tă haɗiye mu, mu ma!”
35 Sai wuta ta fito daga wurin UBANGIJI ta cinye mutane 250 da suke miƙa hadaya
da turare.
36 UBANGIJI ya ce wa Musa, 37 “Ka gaya wa Eleyazar ɗan Haruna, firist, yă kawar
da farantan ƙona turare daga wurin da wutar ta cinye, yă watsar da gawayin a wani
wuri, gama farantan tsarkakakku ne, 38 gama an yi amfani da farantan don miƙa
mini turare. Sai ka ɗauki farantan mutanen da suka yi zunubin da ya jawo musu
mutuwa ka ƙera farantan, ka yi murfin bagade da su, gama an miƙa su a gaban
UBANGIJI, suka zama tsarkakakku. Bari su zama alama ga Isra'ilawa.”
39 Haka Eleyazar, firist, ya tattara farantan tagulla waɗanda mutanen da aka hallaka
suka kawo, ya ƙera murfin bagade da su, 40 yadda UBANGIJI ya umarce shi, ta wurin
Musa. Wannan ya zama abin tuni ga Isra'ilawa domin kada wani da ba firist ba,
bai kuwa fito a cikin zuriyar Haruna ba, yă zo don yă ƙona turare a gaban UBANGIJI,
domin kada yă zama kamar Kora da mabiyansa.
41 Kashegari dukan taron Isra'ilawa suka yi gunaguni a kan Musa da Haruna suka
ce, “Kun kashe mutanen UBANGIJI.”
42 Bayan haka, sai dukan jama'a suka taru domin su nuna rashin yardansu da abin
da suke zato Musa da Haruna ne suka aikata. Da suka fuskanci Tentin Sujada, nan
take sai girgije ya rufe shi, ɗaukaka UBANGIJI kuwa ta bayyana. 43 Sai Musa da Haruna
suka je gaban Tentin Sujada, 44 UBANGIJI kuma ya ce wa Musa, 45 “Ku nisanci wannan
taro, gama yanzu nan zan hallaka su.” Sai Musa da Haruna suka fāɗi rubda ciki.
46 Sai Musa ya ce wa Haruna, “Ka ɗauki farantinka ka sa turare a ciki, da wuta daga
bagade, ka yi maza ka tafi wajen taron, ka yi kafara dominsu. Gama fushin UBANGIJI
ya riga ya sauko; an kuma fara annoba.” 47 Saboda haka Haruna ya yi kamar yadda
Musa ya faɗa, ya ruga a guje zuwa tsakiyar taron. An riga an fara annobar a cikin
mutane, amma Haruna ya miƙa turaren ya kuma yi kafara dominsu. 48 Ya tsaya
tsakanin matattu da masu rai, annobar kuwa ta tsaya. 49 Amma mutane 14,700 ne
suka mutu a annobar, ban da waɗanda suka mutu a sanadin Kora. 50 Sai Haruna ya
komo wurin Musa a ƙofar Tentin Sujada, gama annobar ta ƙare.

# 17

*Tohuwar sandar Haruna*

1 UBANGIJI ya ce wa Musa, 2 “Ka yi magana da Isra'ilawa, ka kuma karɓi sanduna
goma sha biyu daga wurinsu, sanda guda daga kowane shugaban gidan kakanninsu.
Ka rubuta sunan kowa a sandansa. 3 A kan sandan Lawi kuwa ka rubuta sunan
Haruna, gama dole a sami sanda ɗaya saboda shugaban gidan kakanninsu. 4 Ka
ajiye su a Tentin Sujada, a gaba akwatin Alkawari, inda zan sadu da kai. 5 Sandan
mutumin da na zaɓa zai yi toho, da haka zan raba kaina da gunagunin da Isra'ilawa
suke yi.”
6 Saboda haka Musa ya yi magana da Isra'ilawa, sai shugabanninsu suka ba shi
sanduna goma sha biyu, sanda ɗaya don shugaba, bisa ga gidajen kakanninsu, sandan
Haruna kuma yana a cikinsu. 7 Sai Musa ya ajiye sandunan a gaban UBANGIJI a cikin
Tentin Sujada.
8 Kashegari da Musa ya shiga cikin Tentin Sujada sai ga sandan Haruna na gidan
Lawiyawa ya yi toho, ya yi furanni, ya kuma yi 'ya'yan almon. 9 Sai Musa ya fitar wa
dukan Isra'ilawa dukan sandunan da suke daga gaban UBANGIJI. Suka duba, kowa
kuma ya ɗauki sandansa.
10 UBANGIJI ya ce wa Musa, “Ka mayar da sandan Haruna a akwatin Alkawari, don
a ajiye shi alama ga masu tawaye. Wannan zai kawo ƙarshen gunaguninsu a kaina,

domin kada su mutu.” 11 Musa kuwa ya aikata kamar dai yadda UBANGIJI ya umarce
shi.
12 Sai Isra’ilawa suka ce wa Musa, “To, ai in haka ne, mun ƙare ke nan! 13 Idan an
ce duk wanda ya zo kusa da tabanakul na UBANGIJI zai mutu, ai rayuwarmu kamar
mun mutu ke nan.”

# 18

### *Ayyukan da suka shafi firistoci da Lawiyawa*

1 UBANGIJI ya ce wa Haruna, “Kai da ’ya’yanka, da kuma iyalin mahaifinka za ku
ɗauki hakkin abin da ya shafi Tentin Sujada, kai da ’ya’yanka kaɗai za ku ɗauki
hakkin aikinku wanda ya shafi firistoci. 2 Ka kawo ’yan’uwanka Lawiyawa daga
kabilar kakanka tare da kai, don su taimake ka sa’ad da kai da ’ya’yanka kuke hidima
a gaban Tentin Sujada. 3 Za su kasance a ƙarƙashinka, su ne kuma za su yi dukan
hidima ta Tenti, amma kada su je kusa da kayayyakin wuri mai tsarki, ko bagade,
in ba haka ba, da kai da su, za ku mutu. 4 Za su haɗa hannu tare da kai su ɗauki
nauyin lura da Tentin Sujada, dukan ayyuka a Tenti, ba kuma wanda zai zo kusa da
inda kake.
5 “Kai ne za ka ɗauki nauyin lura da wuri mai tsarki da bagade, domin kada fushi
yǎ sāke fāɗa a kan Isra’ilawa. 6 Ni da kaina na zaɓo ’yan’uwanka Lawiyawa daga
cikin Isra’ilawa a matsayin kyauta a gare ku, keɓaɓɓu don UBANGIJI, domin su yi
hidima a Tentin Sujada. 7 Amma kai ne kaɗai da ’ya’yanka za ku yi aiki a matsayin
firistoci game da kowane abu a Tentin Sujada da kuma bayan labule. Ina ba ka aikin
firist, yǎ zama naka. Duk wani kuma da ya zo kusa da wuri mai tsarki, dole a kashe
shi.”

### *Hadayu domin firistoci da Lawiyawa*
### *(Maimaitawar Shari’a 18.1-8)*

8 Sai UBANGIJI ya ce wa Haruna, “Na ba ka aikin lura da hadayun da za a miƙa mini,
dukan tsarkakan hadayun da Isra’ilawa suka ba ni, na ba ka su su zama rabonka da
na ’ya’yanka har abada. 9 Kai za ka riƙe sashe mafi tsarki na hadayun da suka ragu
daga wuta. Daga dukan kyautai mafi tsarki na hadayun da suka miƙa mini, ko ta
gari, ko don zunubi, ko kuma don laifi, wannan kashi naka ne da ’ya’yanka. 10 Ku ci
shi a matsayin abu mafi tsarki; kowane namiji zai ci. Dole ku ɗauke shi da tsarki.
11 “Har yanzu kuma duk abin da aka keɓe daga kyautai na dukan hadayun kaɗawa
na Isra’ilawa naka ne. Na ba da wannan gare ka da ’ya’yanka maza da mata, a
kowane lokaci. Kowa da yake da tsarki a gidanka zai iya ci.
12 “Na ba ka duk man zaitun mafi kyau, da ruwan inabi mafi kyau duka, da hatsi
mafi kyau duka na nunan farinsu da suke bayarwa ga UBANGIJI. 13 Dukan nunan
fari na ƙasar da suke kawo wa UBANGIJI, zai zama naka. Kowa da yake da tsarki a
gidanka zai iya ci.
14 “Kome a Isra’ila da aka keɓe wa UBANGIJI, zai zama naka. 15 Kowane haihuwar
fari, ta mutum, ko ta dabba da suka miƙa wa UBANGIJI, naka ne. Amma ka fanshi
kowace haihuwar fari ta mutum, ko ta dabbar da take haram. 16 Sa’ad da suke wata
ɗaya da haihuwa, dole a fanshe su a bakin shekel biyar-biyar, bisa ga ma’aunin shekel
na tsattsarkan wuri da ake amfani da shi, wanda nauyinsa ya kai gera ashirin.
17 “Amma kada ka fanshe ɗan fari na saniya, tunkiya, ko akuya; gama suna da
tsarki. Ka yayyafa jininsu a bisan bagade, ka kuma ƙone kitsensu kamar hadayar
da ka yi da wuta, mai daɗin ƙanshi ga UBANGIJI. 18 Namansu zai zama naka,
haka ma ƙirji na kaɗawa da cinyar dama za su zama naka. 19 Kome da aka keɓe
daga tsarkakakku hadayun da Isra’ilawa suka miƙa wa UBANGIJI, na ba ka, da kai

da ’ya’yanka maza da mata a matsayin zaunannen rabo. Wannan madawwamin
alkawarin gishiri ne a gaban UBANGIJI dominka da zuriyarka.”
[20] UBANGIJI ya ce wa Haruna, “Ba ka da gādo a ƙasarsu, ba kuwa za ka sami rabo
daga cikinsu ba; ni ne rabonka da gādonka a cikin Isra’ilawa.
[21] “Na ba wa Lawiyawa dukan zakka na Isra’ilawa a matsayin gādonsu, saboda
aikin da suke yi yayinda suke hidima a Tentin Sujada. [22] Daga yanzu zuwa gaba,
kada Isra’ilawa su yi kusa da Tentin Sujada, in ba haka ba ba kuwa su sha hukuncin
zunubinsu, su kuma mutu. [23] Lawiyawa ne za su yi aikin Tentin Sujada, su
kuma ɗauki nauyin kowane laifin da aka aikata a wurin. Wannan za tă zama
dawwammamiyar farilla ce daga yanzu har tsararraki masu zuwa. Ba za su sami
gādo a cikin Isra’ilawa ba. [24] A maimako haka, na ba wa Lawiyawa zakka da
Isra’ilawa suka kawo domin hadaya ga UBANGIJI, a matsayin gādonsu. Shi ya sa
na ce game da su, ‘Ba su da gādo a cikin Isra’ilawa.’ ”
[25] UBANGIJI ya ce wa Musa, [26] “Ka yi wa Lawiyawa magana, ka ce musu, ‘Sa’ad da
kuka karɓi zakka daga Isra’ila da na ba ku gādo, dole ku miƙa kashi ɗaya bisa goma
na wannan zakka a matsayin hadaya ga UBANGIJI. [27] Za a lissafta hadayarku kamar
hatsin da aka sussuka daga masussuka, ko ruwan inabi daga wurin matsewar inabi.
[28] Ta haka za ku miƙa hadaya ga UBANGIJI daga cikin dukan zakkar da kuka karɓa
daga wurin Isra’ilawa. Daga waɗannan zakka kuwa dole ku ba Haruna firist rabon
UBANGIJI. [29] Dole ku miƙa wa UBANGIJI rabo mafi kyau da kuma sashi mafi tsarki na
kowane abin da aka ba ku.’
[30] “Ka faɗa wa Lawiyawa cewa, ‘Sa’ad da kuka miƙa sashi mafi kyau, za a lissafta
shi a matsayin abin da ya fito daga masussuka, ko wurin matsewar ruwan inabi ne.
[31] Da kai da gidanka, za ku iya cin abin da ya rage a ko’ina, gama ladan aikinku ne
a Tentin Sujada. [32] Ta wurin miƙa masa sashi mafi kyau, ba za ku zama masu laifi a
wannan batu ba; ta haka ba za ku ƙazantar da tsarkakakkun hadayu na Isra’ilawa
ba, ba kuwa za ku mutu ba.’ ”

# 19

*Ruwan tsarkakewa*

[1] UBANGIJI ya ce wa Musa da Haruna, [2] “Wannan ita ce ƙa’ida wadda UBANGIJI ya
umarta. Faɗa wa Isra’ilawa su kawo maka jan karsana marar lahani, ko marar aibi
wadda ba a taɓa sa ta tă yi noma ba. [3] Ka ba wa Eleyazar firist; a kuma kai ta
bayan sansani, a yanka a gaban Eleyazar. [4] Sa’an nan Eleyazar firist zai ɗiba jininta
a yatsarsa, yă yayyafa sau bakwai wajen gaban Tentin Sujada. [5] Sa’an nan a ƙone
dukan karsanar, haɗe da fatarta, naman, jinin da kayan cikin, yayinda Eleyazar yake
kallo. [6] Firist zai ɗauki itacen al’ul, da hizzob, da jan ulu, yă jefa su a kan karsanar da
ake ƙonewa. [7] Bayan haka, dole firist yă wanke rigunarsa, yă kuma yi wanka. Sa’an
nan zai iya shiga cikin sansani, amma zai kasance da ƙazanta har yamma. [8] Dole
mutumin da ya ƙone ta yă wanke rigunarsa, yă kuma yi wanka, shi ma zai kasance
da ƙazanta har yamma.
[9] “Mutumin da yake da tsarki, zai tara tokar karsanar, yă sa ta a wurin da yake da
tsabta a bayan sansani. Jama’ar Isra’ilawa ne za su adana shi don amfani a ruwan
tsabtaccewa; wannan domin tsarkakewa ne daga zunubi. [10] Dole mutumin da ya
tara tokar karsanar yă wanke rigunarsa, zai kuwa kasance da ƙazanta har yamma.
Wannan za tă zama dawwammamiyar farilla ta har abada ga Isra’ilawa, da kuma
baƙin da suke zama a cikinsu.
[11] “Duk wanda ya taɓa gawa, zai kasance da ƙazanta har kwana bakwai. [12] Dole yă
tsarkake kansa da ruwa a rana ta uku, da kuma a rana ta bakwai; sa’an nan zai zama
da tsarki. Amma in bai tsarkake kansa a rana ta uku da kuma a rana ta bakwai ba, ba

zai kasance da tsarki ba. 13 Duk wanda ya taɓa gawar wani, bai kuma tsarkake kansa
ba, ya ƙazantar da tabanakul na UBANGIJI ke nan. Dole a ware wannan mutum daga
cikin Isra'ilawa. Gama ba a yayyafa ruwan tsabtaccewa a kansa ba; ya ƙazantu, ya
kasance da ƙazanta ke nan.
14 "Ga ƙa'idar da za a bi in mutum ya mutu a cikin tenti. Duk wanda ya shiga
tentin, kuma duk wanda yake cikinsa, za su zama da ƙazanta har kwana bakwai,
15 kuma kowane abin da ake zuba kaya, wanda ba shi da murfi a kansa, zai zama da
ƙazanta.
16 "Wanda duk yake a fili, ya kuma taɓa gawa wanda aka kashe da takobi, ko wanda
ya mutu mutuwar Allah, ko ƙashin mutum, ko kabari, zai ƙazantu har bakwai.
17 "Ga wanda ya ƙazantu kuwa, a ɗiba toka daga hadaya ta ƙonawa ta tsarkakewa,
a zuba a cikin tulu, sa'an nan a zuba ruwa mai gudu a kansu. 18 Sa'an nan wanda
yake tsarkakakke, zai ɗauki hizzob yă tsoma a ruwa, yă yayyafa a tentin da dukan
kayayyakinsa, da kuma a kan mutanen da suke wurin. Dole kuma yă yayyafa ruwan
a kan duk wanda ya taɓa ƙashin mutu, ko kabari, ko kuma wanda aka kashe, ko
wanda ya yi mutuwa ta Allah. 19 A rana ta uku, da ta bakwai kuma mai tsarkakewa
zai yayyafa wa marar tsarkin ruwa, a rana ta bakwai kuma yă tsarkake shi. Wanda
aka tsarkaken kuwa, dole yă wanke rigunarsa, yă kuma yi wanka da yamma, zai
kuma tsarkaka. 20 Amma in wanda yake da ƙazanta bai tsarkake kansa ba, dole a
ware shi daga cikin jama'a, domin ya ƙazantar da wuri mai tsarki na UBANGIJI. Ba a
yayyafa masa ruwa na tsarkakewa ba, ya zama da ƙazanta. 21 Wannan za tă zama
musu dawwammamiyar farilla.
"Mutumin da ya yayyafa ruwa na tsarkakewa, shi ma dole yă wanke rigarsa. Duk
wanda kuma ya taɓa ruwan tsarkakewa, zai kasance da ƙazanta har yamma. 22 Duk
abin da mai ƙazanta ya taɓa, ya ƙazantu, kowa kuma ya taɓa wannan abu, ya
ƙazantu ke nan, har yamma."

# 20

*Ruwa daga dutse*

1 A watan fari, dukan jama'ar Isra'ilawa suka iso Hamadan Zin. Suka sauka a
Kadesh. A nan ne Miriyam ta mutu, aka kuma bizne ta.
2 Sai aka rasa ruwa da jama'a za su sha, mutane suka taru, suka tayar wa Musa
da Haruna. 3 Suka yi gunaguni wa Musa suka ce, "Da ma mun mutu sa'ad da
'yan'uwanmu suka mutu a gaban UBANGIJI! 4 Don me ka kawo jama'ar UBANGIJI
a wannan hamada, don mu da dabbobinmu mu mutu a nan ke nan? 5 Don me ka
fitar da mu daga Masar zuwa wannan banzan wuri, inda babu hatsi ko ɓaure, inabi
ko rumman. Kuma babu ruwan da za a sha?"
6 Sai Musa da Haruna suka tashi daga taron, suka tafi ƙofar Tentin Sujada, suka
fāɗi rubda ciki, sai ɗaukakar UBANGIJI ta bayyana musu. 7 UBANGIJI ya ce wa Musa,
8 "Ka ɗauki sandanka, kai da Haruna, ɗan'uwanka, ku tara jama'a, ku yi magana da
dutsen a gabansu ya ba da ruwan da yake cikinsa. Za ka sa ruwa ya ɓuɓɓugo musu
daga dutsen. Ta haka za ka ba taron jama'a da garkunansu ruwan sha."
9 Sai Musa ya je ya ɗauki sandan kamar yadda UBANGIJI ya umarce shi. 10 Shi da
Haruna, suka tara jama'a a gaban dutsen, Musa ya ce musu, "Ku saurara, ku 'yan
tawaye, dole mu kawo muku ruwa daga wannan dutse?" 11 Sai Musa ya ɗaga hannu,
ya bugi dutsen sau biyu da sandansa. Ruwa kuwa ya yi ta kwararowa, jama'a da
dabbobinsu suka sha.
12 Amma UBANGIJI ya ce wa Musa da Haruna. "Tun da yake ba ku gaskata ni ba, ba
ku kuwa ɗaukaka ni a idon Isra'ilawa ba, to, ba za ku kai taron jama'an nan a ƙasar
da na ba su ba."

13 Waɗannan su ne ruwan Meriba,* inda Isra'ilawa suka yi wa UBANGIJI gunaguni,
inda kuma ya nuna kansa mai tsarki a cikinsu.

### *Edom ya hana Isra'ila wucewa*

14 Musa ya aiki manzanni daga Kadesh zuwa wurin sarkin Edom cewa,
"Ga abin da ɗan'uwanka Isra'ila ya ce ka san duk irin wahalolin da ya same
mu. 15 Kakanninmu sun gangaro zuwa Masar, muka zauna can shekaru da yawa.
Masarawa suka wulaƙanta mu, da kuma kakanninmu, 16 amma da muka yi kuka
a gaban UBANGIJI, ya kuwa ji mu, sai ya aiko mala'ika, ya fitar da mu daga Masar.
"Yanzu ga mu a Kadesh, garin da yake kan iyakar yankinka. 17 Muna roƙonka,
ka yarda mana mu bi ta ƙasarka. Ba za mu bi ta wani fili, ko gonar inabi ba, ko
mu sha ruwa daga wata rijiya ba. Za mu bi ta babban hanyar sarki, ba kuwa za
mu kauce dama, ko hagu ba, har mu wuce yankinka."
18 Amma Edom ya amsa ya ce,
"Ba za ku bi ta nan ba; in kuka kuskura, za mu fito, mu yaƙe ku da takobi."
19 Sai Isra'ilawa suka amsa, suka ce,
"Za mu bi ta babbar hanya, in mu, ko dabbobinmu suka sha ruwanku, za mu
biya. Mu dai muna so mu wuce ne kawai."
20 Sai mutanen Edom suka sāke amsa suka ce,
"Ba za ku bi nan ba dai."
Sai Edom ya fito da runduna mai ƙarfi da yawa gaske a kan Isra'ila. 21 Da yake
Edom suka ƙi su bar su su ratsa yankinsu, sai Isra'ila suka juya suka janye daga gare
su.

### *Mutuwar Haruna*

22 Dukan Jama'ar Isra'ilawa suka tashi daga Kadesh, suka zo Dutsen Hor. 23 A
Dutsen Hor, kusa da iyakar Edom, UBANGIJI ya ce wa Musa da Haruna, 24 "Haruna
zai rasu. Ba zai shiga ƙasar da na ba Isra'ilawa ba, domin ku biyu, kun ƙi ku bi
umarnina a ruwan Meriba. 25 Ka kawo Haruna da ɗansa Eleyazar, ka kai su a bisan
Dutsen Hor. 26 Ka tuɓe taguwar Haruna ka sa wa ɗansa Eleyazar, gama Haruna zai
rasu a can."
27 Musa ya yi yadda UBANGIJI ya umarta. Suka hau Dutsen Hor a idon dukan jama'a.
28 Musa ya tuɓe taguwar Haruna, ya kuma sa wa Eleyazar ɗan Haruna. Nan kuwa
Haruna ya mutu a bisa dutsen. Sa'an nan Musa da Eleyazar suka sauka daga dutsen,
29 sa'ad da dukan jama'a kuwa suka ji cewa Haruna ya mutu, sai dukan gidan Isra'ila
suka yi makoki dominsa har kwana talatin.

## 21

### *An hallaka Arad*

1 Sa'ad da sarkin Arad, mutumin Kan'ana, wanda yake zaune a Negeb, da ya ji
cewa Isra'ila yana zuwa ta hanyar Atarim, sai ya fito, yǎ yaƙi Isra'ilawa, yǎ kuma
kama waɗansunsu. 2 Sai Isra'ila suka yi alkawari wa UBANGIJI suka ce, "In ka ba da
waɗannan mutane a hannunmu, za mu hallaka dukan garuruwansu ƙaf." 3 UBANGIJI
kuwa ya saurari kukan Isra'ila, ya kuma ba da Kan'aniyawa a gare su. Suka hallaka
su da biranensu ƙaf; saboda haka aka sa wa wurin suna Horma.*

### *Macijin tagulla*

4 Suka kama hanya daga Dutsen Hor ta hanya zuwa Jan Teku, don su kauce wa
Edom. Amma mutane suka rasa haƙuri a hanya; 5 suka yi wa Allah da Musa gunaguni,
suka ce, "Me ya sa kuka fitar da mu daga Masar, kuka kawo mu mu mutu a wannan

* **20:13** Meriba yana nufin faɗa. * **21:3** Horma yana nufin hallaka.

hamada? Babu abinci! Babu ruwa! Mu dai mun gaji da wannan abinci marar
amfani!”
6 Sai Ubangiji ya aiko da macizai masu dafin a cikinsu, suka sassari mutane,
Isra’ilawa masu yawa kuwa suka mutu. 7 Mutanen suka zo wurin Musa, suka ce,
“Mun yi zunubi, da muka yi wa Ubangiji da kai gunaguni. Ka yi addu’a don Ubangiji
yǎ ɗauke mana macizan nan.” Saboda haka Musa ya yi addu’a domin mutane.
8 Ubangiji ya ce wa Musa, “Ka ƙera siffar maciji ka rataye shi a bisa doguwar sanda;
kowa da maciji ya sare shi, idan ya dubi macijin nan da ka rataye, zai rayu.” 9 Saboda
haka Musa ya ƙera macijin tagulla, ya kuma rataye shi bisa doguwar sanda. Sa’an
nan duk wanda maciji ya sare shi, ya kuma dubi macijin tagullar, zai warke.

### *Tafiya zuwa Mowab*

10 Isra’ilawa suka kama hanya, suka yi sansani a Obot. 11 Sai suka tashi daga Obot,
suka yi sansani a Iye Abarim a hamadar da take fuskantar Mowab, wajen fitowar
rana. 12 Daga nan kuma suka ci gaba, suka yi sansani a Kwarin Zered. 13 Suka
tashi daga nan, suka sauka kusa da Arnon wanda yake a hamadar da ta miƙe zuwa
iyakar Amoriyawa. Arnon shi ne iyakar Mowab, wanda yake tsakanin Mowab da
Amoriyawa. 14 Shi ya sa Littafin Yaƙoƙin Ubangiji ya ce,
“Waheb ta cikin yankin Sufa, da kwararuka
na tuddan Arnon, 15 da gangaren kwararuka,
wanda ya nausa zuwa garin Ar,
ya kuma dangana da kan iyakar Mowab.”
16 Daga can, suka gangara zuwa Beyer, wato, rijiyar da Ubangiji ya ce wa Musa, “Ka
tattara mutane duka, zan kuwa ba su ruwa.”
17 Sai Isra’ilawa suka rera wannan waƙa,
“Ki ɓuɓɓugo da ruwa, Ke rijiya!
Rera waƙa game da ita,
18 game da rijiyar da ’ya’yan sarki suka haƙa,
rijiyar da manyan mutane masu sandunan sarauta suka nuna da sandunansu.”
Sa’an nan suka tashi daga hamadar, suka tafi Mattana, 19 daga Mattana, suka tafi
Nahaliyel, daga Nahaliyel, suka tafi Bamot, 20 daga Bamot kuma suka tafi kwarin da
yake cikin Mowab inda ƙwanƙolin Fisga yake fuskantar hamada.

### *An ci Sihon da Og*
### *(Maimaitawar Shari’a 2.26-37)*

21 Isra’ila suka aiki manzanni wurin Sihon sarkin Amoriyawa su ce,
22 “Ka bari mu ratsa ta ƙasarka. Ba za mu shiga wata gona ba, ba za mu kuma
shiga gonar inabi, ko mu sha ruwa daga wata rijiya ba. Za mu bi ta babbar hanyar
sarki, har mu fita ƙasarka.”
23 Amma Sihon bai bar Isra’ila su ratsa ta yankinsa ba. Sai ya tara dukan sojojinsa,
suka fita zuwa cikin hamada, su yaƙi Isra’ila. Da ya kai Yahaz, sai ya yaƙi Isra’ila.
24 Isra’ila fa suka kashe shi da takobi, suka ƙwace ƙasarsa, tun daga kogin Arnon har
zuwa kogin Yabbok, zuwa kan iyakar Ammonawa kawai, gama sun yi wa iyakansu
katanga. 25 Isra’ila suka ci dukan biranen Amoriyawa, suka kuma zauna a cikinsu,
haɗe da babban birnin Heshbon da dukan ƙauyukanta. 26 Sihon sarkin Amoriyawa
ya yi mulkin Heshbon, bayan ya ci sarkin Mowab na dā da yaƙi, ya kuma ƙwace
dukan ƙasarsa har zuwa arewancin kogin Arnon.
27 Shi ya sa Amoriyawa suka rubuta wannan waƙa game da Heshbon suka ce,
“Ku zo mu sāke gina Heshbon,
birnin Sihon.

28 “Mayaƙansa sun fito kamar

harshen wuta
suka ƙone birnin Ar na Mowab
suna hallaka ʼyan ƙasar
tuddan Arnon.
29 Kaitonki, Mowab!
Gunkinki Kemosh
ya yashe mutanenki;
aka kuma kama su, aka kai su bauta
wajen Sihon sarkin Amoriyawa.

30 "Amma mun tumɓuke su,
mun hallaka garuruwan Heshbon har zuwa Dibon.
Mun ragargaza su har zuwa Nofa
wanda ya miƙe zuwa Medeba."

31 Ta haka Isra'ila suka zauna a ƙasar Amoriyawa.

32 Sai Musa ya aika ʼyan leƙen asiri zuwa Yazer. Daga baya, sai Isra'ilawa suka ci
ƙauyukan da suke kewaye, suka kuma kori Amoriyawa da suke zaune a can.

*(Maimaitawar Shari'a 3.1-11)*

33 Sai suka juya suka haura kan hanya ta zuwa Bashan, inda Og yake sarauta, ya
kuwa fito tare da dukan sojojinsa suka yi yaƙi da Isra'ila a Edireyi.

34 UBANGIJI ya ce wa Musa, "Kada ka ji tsoronsa, gama na ba da shi a gare ka,
da dukan sojojinsa da kuma ƙasarsa. Ka yi da shi yadda ka yi da Sihon sarkin
Amoriyawa, wanda ya yi mulki a Heshbon."

35 Ta haka suka kashe shi, tare da ʼyaʼyansa maza da kuma dukan sojojinsa, ba
wanda ya ragu. Suka kuma mamaye ƙasarsa.

# 22

*Balak ya kira Bala'am*

1 Sai Isra'ilawa suka kama hanya, suka tafi filayen Mowab, a wajen Urdun, a ƙetare
Yeriko,* suka yi sansani a can.

2 To, fa, Balak ɗan Ziffor ya ga duk abin da Isra'ila suka yi da Amoriyawa. 3 Sai
Mowab ya firgita ƙwarai saboda yawan mutanen. Tsoron Isra'ilawa ya kama su.

4 Sai Mowabawa suka ce wa dattawan Midiyawa, "Wannan taron zai lashe duk abin
da ya kewaye mu kamar yadda saniya takan lashe ciyawa a fili."

Saboda haka Balak ɗan Ziffor, wanda yake sarkin Mowab a lokacin, 5 ya aika
manzanni su zo da Bala'am ɗan Beyor, wanda yake a Fetor, kusa da Kogi,† a ƙasar
haihuwarsa. Balak ya ce,

"Ga mutane sun fito daga Masar; sun mamaye ƙasar, suka kuma yi sansani kusa
da ni. 6 Ka zo yanzu ka la'anta waɗannan mutane, domin sun fi ƙarfina. Wataƙila
zan iya cin nasara a kansu, in kuma kore su daga ƙasar. Gama na sani duk waɗanda
ka sa musu albarka, sun zama masu albarka ke nan, waɗanda kuma ka la'anta,
sun la'antu ke nan."

7 Sai dattawan Mowab da na Midiyawa suka tashi, suka ɗauki kuɗi don duba. Da
suka zo wurin Bala'am sai suka faɗa masa abin da Balak ya ce.

8 Bala'am ya ce musu, "Ku kwana a nan, ni kuwa zan faɗa muku abin da UBANGIJI
ya faɗa mini." Saboda haka dattawan sarkin Mowab suka zauna da shi.

9 Sai Allah ya zo wurin Bala'am ya ce, "Su wane ne waɗannan tare da kai?"

* **22:1** Da Ibraniyanci Urdun na Yeriko; mai yiwuwa suna na tun dā na Kogin Urdun. † **22:5** Wato, Yuferites.

10 Bala'am ya ce wa Allah, "Balak ɗan Ziffor, sarkin Mowab ne, ya aiko mini wannan
saƙo cewa, 11 'Ga mutane sun fito daga Masar sun mamaye ƙasar. Ka zo yanzu ka
la'anta mini su. Wataƙila ta haka zan yi nasara a kansu, in kuma kore su.' "
12 Amma Allah ya ce wa Bala'am, "Kada ka tafi tare da su. Kada ka la'anta mutanen
nan, gama su masu albarka ne."
13 Kashegari Bala'am ya tashi ya ce wa dattawan Balak, "Ku koma ƙasarku, domin
UBANGIJI ya hana ni in tafi tare da ku."
14 Saboda haka dattawan Mowab suka koma wurin Balak suka ce, "Bala'am ya ƙi
yǎ zo tare da mu."
15 Sai Balak ya aika waɗansu dattawa masu yawa, masu daraja kuma fiye da na
dā. 16 Suka zo wurin Bala'am suka ce,
"Ga abin da Balak ɗan Ziffor ya ce, Kada ka bar wani abu yǎ hana ka zuwa
wurina, 17 gama zan ba ka lada mai yawa in kuma yi duk abin da ka ce. Ka zo ka
la'anta mini waɗannan mutane."
18 Amma Bala'am ya amsa musu ya ce, "Ko da a ce Balak zai ba ni gidansa cike da
azurfa da zinariya, ba zan yi wani abu ko kaɗan saɓanin umarnin UBANGIJI Allahna
ba. 19 To, fa, sai ku kwana a nan kamar yadda waɗancan suka yi, ni kuma in roƙi
UBANGIJI, in ji, wace magana zai ce mini."
20 A wannan dare, Allah ya zo wurin Bala'am ya ce, "Da yake waɗannan mutane
sun zo su tafi da kai, to, ka tafi tare da su, sai dai ka yi abin da na ce ka yi ne kaɗai."

### *Jakin Bala'am*

21 Bala'am ya tashi da safe, ya ɗaura wa jakarsa sirdi, ya tafi tare da dattawan
Mowab. 22 Amma Allah ya husata sa'ad da ya tafi, mala'ikan UBANGIJI kuwa ya tsaya
a hanya don yǎ hana shi. Bala'am kuwa yana kan jakarsa tare da bayinsa biyu. 23 Da
jakar ta hangi mala'ikan UBANGIJI tsaye a hanya da takobi a hannunsa, sai ta kauce
daga hanya, ta shiga jeji. Bala'am kuwa ya buge ta don tǎ koma hanya.
24 Sai mala'ikan UBANGIJI ya tsaya a wata matsattsiyar hanya tsakanin gonaki inabi
biyu, da bango a kowane gefe. 25 Sa'ad da jakar ta ga mala'ikan UBANGIJI, sai ta matse
a jikin bango, ta goge ƙafar Bala'am da bangon. Saboda haka sai Bala'am ya sāke
bugunta.
26 Sai mala'ikan UBANGIJI ya sha gabansa, ya tsaya a ƙunƙuntaccen wuri inda ba
wurin juyawa dama ko hagu. 27 Da jakar ta ga mala'ikan UBANGIJI, sai ta kwanta a
ƙasa, Bala'am kuwa ya husata, sai ya buge ta da sandansa. 28 UBANGIJI ya buɗe bakin
jakar, sai jakar ta ce wa Bala'am, "Me na yi maka da ka buge ni har sau uku?"
29 Bala'am ya ce wa jakar "Domin kin wulaƙanta ni! Da a ce ina da takobi a
hannuna da zan kashe ki nan take."
30 Jakar ta ce wa Bala'am, "Ni ba jakarka ba ce wadda kake hawa kullum, har yǎ
zuwa yau? Na taɓa yin maka haka?"
Bala'am ya ce, "A'a."
31 Sa'an nan UBANGIJI ya buɗe idanun Bala'am, ya kuwa ga mala'ikan UBANGIJI
tsaye a hanya da takobi a zāre. Sai ya sunkuyar da kansa, ya fāɗi rubda ciki.
32 Sa'an nan mala'ikan UBANGIJI ya tambaye shi, "Don me ka buge jakarka har sau
uku? Na fito ne don in hana ka, gama hanyarka ba daidai ba ce a gabana. 33 Jakar
ta gan ni, ta kauce mini har sau uku. Da a ce ba tǎ kauce ba, lalle da na kashe ka, in
kuwa bar ta da rai."
34 Bala'am ya ce wa mala'ikan UBANGIJI, "Na yi zunubi. Ban san ka tsaya a hanya
don ka hana ni ba. Yanzu in ba ka ji daɗin tafiyata, sai in koma."
35 Mala'ikan UBANGIJI ya ce wa Bala'am, "Ka tafi tare da mutanen, amma abin da
na faɗa maka ne kaɗai za ka faɗa." Saboda haka Bala'am ya tafi tare da dattawan
Balak.

36 Da Balak ya ji cewa Bala’am yana zuwa, sai ya fito, ya tarye shi a garin Mowabawa
da suke a iyakar Arnon, a ƙarshen yankinsa. 37 Balak ya ce wa Bala’am, “Ban aika
maka saƙo cikin gagawa ba? Me ya sa ba ka zo ba? Ko ban isa in sāka maka ba ne?”
38 Bala’am ya amsa ya ce, “To, ai, ga shi, na zo yanzu. Ina da wani ikon yin wata
magana ne? Dole in faɗa abin da Allah ya ce in faɗa ne kawai.”
39 Sa’an nan Bala’am ya tafi tare da Balak zuwa Kiriyat-Huzot, 40 a can ya yi hadaya
da shanu da tumaki, ya kuwa aika wa Bala’am da dattawan da suke tare da shi.
41 Kashegari, Balak ya ɗauki Bala’am ya kai shi kan Bamot Ba’al, daga can ya iya
ganin sassan sansanin Isra’ilawa.

# 23

*Maganar Bala’am ta farko na abin da Allah ya faɗa*

1 Bala’am ya ce, “Ka gina mini bagadai bakwai a nan, ka shirya mini bijimai bakwai
da raguna bakwai.” 2 Balak ya yi yadda Bala’am ya faɗa, sai su biyu suka miƙa bijimi
da rago a kan kowane bagade.
3 Sa’an nan Bala’am ya ce wa Balak, “Tsaya nan kusa da hadayarka, ni kuwa in
koma wani wurin da yake a kaɗaice. Wataƙila UBANGIJI zai sadu da ni. Duk abin da
ya bayyana mini, zan faɗa maka.” Sai ya haura kan wani wurin da yake a kaɗaice a
tudun.
4 Allah kuwa ya sadu da Bala’am. Bala’am ya ce, “Na shirya bagadai bakwai, na
kuma miƙa bijimi guda da rago guda, a kan kowane bagade.”
5 UBANGIJI ya ba wa Bala’am saƙo ya ce, “Ka koma wurin Balak, ka faɗa masa
wannan saƙo.”
6 Saboda haka, sai Bala’am ya koma wurin Balak ya same shi tsaye a kusa da
hadayarsa, tare da dukan dattawan Mowab. 7 Sai Bala’am ya furta abin da Allah
ya faɗa masa ya ce,
“Balak ya kawo ni daga Aram,
sarkin Mowab ya kawo ni daga gabashin duwatsu.
Ya ce, ‘Zo, ka la’anta mini Yaƙub;
zo, ka tsine Isra’ila.’
8 Yaya zan iya la’anta
waɗanda Allah bai la’anta ba?
Yaya zan tsine
waɗanda UBANGIJI bai tsine ba?
9 Daga kan duwatsu na gan su,
daga bisa kan tuddai na hange su.
Na ga mutane da suke zaune su kaɗai
ba sa ɗauki kansu ɗaya da al’ummai ba.
10 Wa zai iya ƙidaya ƙurar Yaƙub
ko yă ƙidaya kashi ɗaya bisa huɗu na Isra’ila?
Bari in mutu, mutuwar adali
ƙarshena kuma yă zama kamar nasu!”
11 Balak ya ce wa Bala’am, “Me ke nan ka yi mini? Na kawo ka, ka la’anta abokan
gābana, sai ga shi albarka kake sa musu!”
12 Bala’am ya ce, “Ba dole in faɗa abin da UBANGIJI ya sa a bakina ba?”

*Maganar Bala’am ta biyu na abin da UBANGIJI ya faɗa*

13 Sa’an nan Balak ya ce masa, “Zo, mu tafi wani wuri inda za ka gan su; a nan kana
ganin sashe ne kawai, ba dukansu ba. Daga can kuwa, ka la’anta mini su.” 14 Saboda
haka ya ɗauke shi zuwa filin Zofim a ƙwanƙolin Fisga, a can ya gina bagadai bakwai,
ya kuma miƙa bijimi da rago a kan kowane bagade.

15 Bala'am ya ce wa Balak, "Tsaya nan kusa da hadayarka, ni kuwa in je in sadu da
UBANGIJI a can."
16 UBANGIJI ya sadu da Bala'am, ya kuma ba shi saƙo ya ce, "Koma wurin Balak ka
ba shi wannan saƙo."
17 Saboda haka ya tafi ya same Balak tsaye a kusa da hadayarsa, tare da dattawan
Mowab. Balak ya tambaye Bala'am ya ce, "Mene ne UBANGIJI ya ce?"
18 Sai Bala'am ya furta saƙon da aka ba shi ya ce,
"Tashi, Balak, ka saurara;
ka kasa kunne gare ni, ɗan Ziffor.
19 Allah ba mutum ba ne, da zai yi ƙarya,
shi ba ɗan mutum ba ne, da zai canja tunaninsa.
Yana maganar abin da ba zai iya aikata ba ne?
Yakan kuma yi alkawarin da ba zai iya cikawa ba?
20 Na karɓi umarni in sa albarka;
na kuwa sa albarka, ba zan iya janye ta ba.

21 "Bai ga mugunta a cikin Yaƙub ba,
bai kuma ga wahala a Isra'ila ba.*
UBANGIJI Allahnsu yana tare da su;
sowar Sarki yana cikinsu.
22 Allah ya fitar da su daga Masar;
suna da ƙarfi iri na kutunkun ɓauna.
23 Ba wata maitar da za tă ci Yaƙub,
ba sihiri da zai cuci Isra'ila.
Yanzu za a ce game da Yaƙub
da Isra'ila, 'Duba abin da Allah ya yi!'
24 Mutane sun tashi kamar ƙaƙƙarfar zakanya;
sun tā da kansu kamar zaki
wanda ba ya hutawa
sai ya cinye naman abin da ya kama
ya kuma sha jinin abin da ya kama."
25 Sai Balak ya ce wa Bala'am, "Kada ka la'anta su, kada kuma ka sa musu albarka!"
26 Bala'am amsa ya ce, "Ban faɗa maka zan yi kaɗai abin da UBANGIJI ya ce ba?"

### *Maganar Bala'am ta uku na abin da UBANGIJI ya faɗa*

27 Sai Balak ya ce wa Bala'am, "Zo in kai ka wani wuri. Wataƙila zai gamshi Allah,
yă bari ka la'anta mini su daga can." 28 Balak kuwa ya ɗauki Bala'am zuwa ƙwanƙolin
Feyor, wanda yake fuskantar hamada.
29 Bala'am ya ce, "Ka gina mini bagadai bakwai a nan, ka kuma shirya mini bijimai
bakwai da raguna bakwai." 30 Balak ya yi yadda Bala'am ya ce, ya kuwa miƙa bijimi
da rago a kan kowane bagade.

## 24

1 To, da Bala'am ya ga cewa UBANGIJI yana jin daɗin sa wa Isra'ila albarka, bai
koma wajen sihiri kamar dā ba, amma ya juya fuskarsa wajen hamada. 2 Da Bala'am
ya duba sai ya ga Isra'ila sun yi sansani kabila, kabila, Ruhun Allah kuwa ya sauko
masa, 3 sai ya yi annabcinsa ya ce,
"Maganar Bala'am ɗan Beyor,
saƙon mutumin da idanunsa ke gani sarai,
4 maganar mutumin da ya saurari maganar Allah,

* 23:21 Ko kuwa Bai dubi laifofin Yaƙub ba, ka a sami wani abin da ba daidai ba a cikin Isra'ila

maganar wanda yake ganin wahayi daga Maɗaukaki,*
mutumin da ya fāɗi rubda ciki, wanda kuma idanunsa suna a buɗe.

5 “Ina misalin kyan tentunanka, ya Yaƙub,
wuraren zamanka, ya Isra’ila!

6 “Kamar kwaruruka suke a shimfiɗe,
kamar lambu kusa da rafi,
kamar itatuwan aloyes da UBANGIJI ya dasa,
kamar itatuwa al’ul kusa da ruwaye.
7 Ruwa zai kwararo daga bokitinsu;
irinsu za su sami ruwa a yalwace.

“Sarkinsu zai fi sarkin Agag;
mulkinsu zai ɗaukaka.

8 “Allah ya fitar da su daga Masar;
suna da ƙarfin kutunkun ɓauna.
Sun cinye abokan gāban,
suka kakkarya ƙasusuwansu;
da kibiyoyinsu suka sossoke su.
9 Kamar zaki sun laɓe sun kwanta,
kamar zakanya, wa zai yi ƙarfin hali yǎ tashe su?

“Bari waɗanda suka albarkace ka, su sami albarka
waɗanda kuma suka la’anta ka, su la’antu!”
10 Fushin Balak ya ƙuna a kan Bala’am. Ya tafa hannunsa, ya ce masa, “Na kira
ka don ka la’anta abokan gābana, amma sai ga shi ka sa musu albarka har sau uku.
11 Yanzu ka bar nan ka tafi gida! Na ce zan sāka maka da lada mai kyau, amma
UBANGIJI ya hana ka samun ladan.”
12 Bala’am ya ce wa Balak, “Ban faɗa wa ’yan aikan da ka aiko wurina ba cewa,
13 ‘Ko da a ce Balak zai ba ni gidansa cike da azurfa da zinariya, ba zan yi wani abu
ko kaɗan saɓanin umarnin UBANGIJI Allahna ba, kuma dole in faɗa abin da UBANGIJI
ya ce ne kawai’? 14 Yanzu zan koma wajen mutanena, amma bari in gargaɗe ka game
da abin da mutanen nan za su yi wa mutanenka cikin kwanaki masu zuwa.”

### *Maganar Bala’am ta huɗu na abin da Allah ya faɗa*

15 Sa’an nan ya furta saƙonsa.
“Maganar Bala’am ɗan Beyor,
saƙon mutumin da idanunsa ke gani sarai,
16 maganar mutumin da ya saurari maganar Allah,
wanda yake da sani daga Mafi Ɗaukaka,
wanda yake ganin wahayi daga Maɗaukaki,
wanda ya fāɗi rubda ciki, wanda kuma idanunsa suna a buɗe.

17 “Na gan shi, amma ba yanzu ba;
na hange shi, amma ba kusa ba.
Tauraro zai fito daga Yaƙub;
sandan mulki zai fito daga Isra’ila.
Zai ragargaje goshin Mowab,

* **24:4** Da Ibraniyanci Shaddai; haka ma a aya 16.

kawunan dukan ʼyaʼyan Set.
18 Za a ci Edom da yaƙi;
za a ci Seyir, abokiyar gābanta,
amma Israʼila zai ƙara ƙarfi.
19 Mai mulki zai fito daga Yaƙub
yă hallaka waɗanda suka ragu a birnin."

### *Maganar Balaʼam ta ƙarshe na abin da Allah ya faɗa*

20 Sai Balaʼam ya ga Amalek, ya kuma furta maganarsa.
"Amalek yana cikin alʼummai na fari,
amma zai zama na ƙarshen da za a hallaka."
21 Sai ya ga Keniyawa, ya kuma furta maganarsa.
"Wurin zamanku lafiya yake,
an kuma sa sheƙarku a cikin duwatsu;
22 duk da haka, za a hallaka ku Keniyawa
saʼad da Asshur ya kame ku."
23 Sai ya furta maganarsa ya ce,
"Wayyo, wa zai rayu saʼad da Allah ya yi haka?
24 Jiragen ruwa za su zo daga Kittim;
za su murƙushe Asshur da Eber,
amma su ma za a hallaka su."
25 Saʼan nan Balaʼam ya tashi ya koma gidan, Balak kuma ya yi tafiyarsa.

## 25

### *Mowab sun rinjaye Israʼila*

1 Lokacin da Israʼila suke a sansani a Shittim, sai maza suka fara yin lalata da matan
Mowabawa, 2 waɗanda suka gayyace su zuwa wajen hadayu na allolinsu. Mutane
suka ci suka kuma yi wa waɗannan alloli sujada. 3 Ta haka Israʼila suka sa kai a
bautar gumaka Baʼal-Feyor. UBANGIJI kuwa ya husata da su.
4 UBANGIJI ya ce wa Musa, "Ka kama dukan shugabannin mutanen nan, ka kashe
su, ka kuma bar su a tsakar rana a gaban UBANGIJI, don UBANGIJI yă huce daga fushin
da nake yi da Israʼila."
5 Saboda haka Musa ya ce wa alƙalan Israʼila, "Dole kowannenku yă kashe mutanen
nan da suka haɗa kai cikin bautar Baʼal-Feyor."
6 Saʼan nan wani mutumin Israʼila ya kawo wata Bamidiyana a iyalinsa a idon
Musa da dukan taron jamaʼar Israʼila, yayinda suke kuka a ƙofar Tentin Sujada. 7 Da
Finehas ɗan Eleyazar, ɗan Haruna, firist, ya ga haka, sai ya bar taron, ya ɗauki māshi
8 ya bi mutumin Israʼilan nan cikin tenti, ya soke dukansu biyu, māshin ya ratsa jikin
mutumin Israʼilan har zuwa jikin macen. Saʼan nan aka tsai da annoban nan a kan
Israʼilawa. 9 Waɗanda suka mutu a wannan annoba, sun kai mutum 24,000.
10 UBANGIJI ya ce wa Musa, 11 "Finehas ɗan Eleyazar, ɗan Haruna, firist, ya kawar
da fushina daga Israʼilawa; saboda ya yi kishi irin nawa a gabansu, don haka saboda
ɗaukakata ban kawo ƙarshensu ba. 12 Saboda haka ka faɗa masa cewa zan yi
alkawarin salama da shi. 13 Shi da zuriyarsa za su kasance da alkawari na zama
firist har abada, saboda kishinsa domin ɗaukakar Allahnsa, ya kuma yi kafara domin
Israʼilawa."
14 Sunan mutumin Israʼilan da aka kashe tare da macen nan Bamidiyana kuwa
Zimri ne, ɗan Salu, shugaban mutanen Simeyon. 15 Sunan macen nan Bamidiyana
da aka kashe kuwa Kozbi ne, ʼyar Zur, wani basaraken iyalin Midiyawa.
16 UBANGIJI ya ce wa Musa, 17 "Ka ɗauki Midiyawa a matsayin abokan gāba, ka
kuma kashe su, 18 gama sun ɗauke ku a matsayin abokan gāba, saʼad da suka ruɗe

ku a kan al'amuran Feyor da 'yar'uwarsu Kozbi 'yar shugaban Midiyawa, macen da aka kashe a annoba ta dalili Feyor."

# 26

*Kidaya ta biyu*

1 Bayan annobar, sai UBANGIJI ya yi magana da Musa da Eleyazar ɗan Haruna, firist
ya ce, 2 "Ku ƙidaya dukan jama'ar Isra'ila daga mai shekaru ashirin zuwa gaba da za
su iya aikin sojan Isra'ila." 3 Musa da Eleyazar firist suka yi musu magana a filayen
Mowab kusa da Urdun daga ƙetaren Yeriko, suka ce, 4 "Ku ƙidaya maza daga mai
shekara ashirin zuwa gaba yadda UBANGIJI ya umarci Musa."

Waɗannan su ne Isra'ilawan da suka fito daga Masar.

5 Zuriyar Ruben ɗan fari na Isra'ila,
daga Hanok; kabilar Hanokawa;
daga Fallu; kabilar Falluyawa;
6 daga Hezron, kabilar Hezronawa;
daga Karmi, kabilar Karmiyawa.
7 Waɗannan su ne kabilan Ruben; jimillarsu ta kai 43,730.
8 Ɗan Fallu kuwa shi ne Eliyab, 9 'ya'yan Eliyab maza kuwa su ne, Nemuwel,
Datan da Abiram. Datan da Abiram nan, su ne shugabannin mutanen da suka
tayar wa Musa da Haruna, suna kuma cikin waɗanda suka bi Kora sa'ad da
ya tayar wa UBANGIJI. 10 Kasa kuwa ta buɗe ta haɗiye su tare da Kora, wanda
ƙungiyarsa ta mutu sa'ad da wuta ta cinye mutum 250. Wannan kuwa ya zama
alamar faɗakarwa. 11 Amma fa, zuriyar Kora ba tă mutu ba.

12 Zuriyar Simeyon bisa ga kabilansu,
daga Nemuwel, kabilar Nemuwelawa;
daga Yamin, kabilar Yaminawa;
daga Yakin, kabilar Yakinawa;
13 daga Zera, kabilar Zerawa;
daga Sha'ul, kabilar Sha'ul.
14 Waɗannan su ne kabilan Simeyon; jimillarsu ta kai 22,200.

15 Zuriyar Gad bisa ga kabilansu,
daga Zafon, kabilar Zafonawa;
daga Haggi, kabilar Haggiwa;
daga Shuni, kabilar Shunawa;
16 daga Ozni, kabilar Ozniyawa
daga Eri, kabilar Eriyawa;
17 daga Arod, kabilar Arodiyawa;
daga Areli, kabilar Areliyawa.
18 Waɗannan su ne kabilan Gad, jimillarsu ta kai 40,500.

19 Er da Onan, 'ya'yan Yahuda ne, amma sun mutu a Kan'ana.
20 Zuriyar Yahuda bisa ga kabilansu,
daga Shela, kabilar Shelayawa
daga Ferez, kabilar Ferezawa;
daga Zera, kabilar Zerawa;
21 Zuriyar Ferez kuwa,

daga Hezron, kabilar Hezronawa;
daga Hamul; kabilar Hamulawa.
22 Waɗannan su ne kabilan Yahuda; jimillarsu ta kai 76,500.

23 Zuriyar Issakar bisa ga kabilansu,
daga Tola, kabilar Tolatawa;
daga Fuwa, kabilar Fuwayawa;
24 daga Yashub, kabilar Yashubawa;
daga Shimron, kabilar Shimronawa.
25 Waɗannan su ne kabilan Issakar; jimillarsu ta kai 64,300.

26 Zuriyar Zebulun bisa ga kabilansu,
daga Sered, kabilar Seredawa;
daga Elon kabilar Elonawa;
daga Yaleyel; kabilar Yaleyewa.
27 Waɗannan su ne kabilan Zebulun, jimillarsu ta kai 60,500.

28 Zuriyar Yusuf bisa ga kabilansu ta wurin Manasse da Efraim.
29 Zuriyar Manasse,
daga Makir, kabilar Makiriyawa (Makir shi ne mahaifin Gileyad);
daga Gileyad, kabilar Gileyadawa.
30 Waɗannan su ne zuriya Gileyad,
daga Iyezer, kabilar Iyezerawa;
daga Helek, kabilar Helekawa;
31 daga Asriyel, kabilar Asriyelawa;
daga Shekem, kabilar Shekem;
32 daga Shemida, kabilar Shemadawa;
daga Hefer, kabilar Heferawa.
33 (Zelofehad ɗan Hefer, ba shi da ʼyaʼya maza; ʼyan mata ne kaɗai ya haifa,
sunayensu kuwa su ne Mala, Nowa, Hogla, Milka da Tirza.)
34 Waɗannan su ne kabilan Manasse, jimillarsu ta kai 52,700.
35 Waɗannan su ne kabilan Efraim bisa ga kabilansu,
daga Shutela, kabilar Shutelawa;
daga Beker, kabilar Bekerawa;
daga Tahan, kabilar Tahanawa.
36 Waɗannan su ne kabilan Shutelawa,
daga Eran, kabilar Eranawa.
37 Waɗannan su ne kabilan Efraim; jimillarsu ta kai 32,500.
Waɗannan su ne kabilan Yusuf ta wurin kabilansu.

38 Zuriyar Benyamin bisa ga kabilansu,
daga Bela, kabilar Belawa;
daga Ashbel, kabilar Ashbelawa;
daga Ahiram, kabilar Ahiramawa;
39 daga Shufam, kabilar Shufamawa;
daga Hufam, kabilar Hufamawa.
40 Zuriyar Bela daga Ard da Naʼaman,
daga Ard, kabilar Ardawa;
daga Naʼaman, kabilar Naʼamawa;
41 Waɗannan su ne kabilan Benyamin, jimillarsu ta kai 45,600.

42 Waɗannan su ne kabilan Dan bisa ga kabilarsu,
daga Shuham, kabilar Shuhamawa.
Waɗannan su ne kabilan Dan. 43 Dukansu kabilan Shuhamawa ne, jimillarsu
ta kai 64,400.

44 Zuriyar Asher bisa ga kabilansu,
daga Imna, kabilar Imnawa
daga Ishbi, kabilar Ishbiyawa;
daga Beriya, kabilar Beriyawa;
45 daga zuriyar Beriya kuwa,
daga Heber, kabilar Heberawa;
daga Malkiyel, kabilar Malkiyelawa.
46 (Asher yana da ʼya mace da ake kira Sera.)
47 Waɗannan su ne kabilan Asher; jimillarsu ta kai 53,400.

48 Zuriyar Naftali bisa ga kabilansu,
daga Yazeyel, kabilar Yazeyelawa;
daga Guni, kabilar Guniyawa;
49 daga Yezer, kabilar Yezerawa;
daga Shillem, kabilar Shillemawa.
50 Waɗannan su ne kabilan Naftali, jimillarsu ta kai 45,400.

51 Dukan jimillar mazan Isra'ila ta kai 601,730.

52 UBANGIJI ya ce wa Musa, 53 "Ka rarraba musu ƙasar a matsayin gādo, bisa ga
yawan kabila. 54 Ga ƙungiya mafi girma, ka ba ta rabo mafi girma; ga ƙaramar
ƙungiya kuwa, ka ba ta ƙarami rabo; kowane zai karɓa rabonsa ga yawan mutanen
da aka rubuta. 55 Ka tabbatar an rarraba ƙasar ta wurin rabo. Abin da kowace
ƙungiya ta gāda zai zama bisa ga sunayen kabilar kakanninta. 56 Za a raba kowane
gādo bisa ga rabo tsakanin manyan da ƙanana ƙungiyoyi."

57 Waɗannan su ne Lawiyawa da a ƙidaya bisa ga kabilansu,
daga Gershom, kabilar Gershonawa;
daga Kohat, kabilar Kohatawa;
daga Merari, kabilar Merari.
58 Waɗannan kuma su ne kabilan Lawiyawa,
kabilar Libniyawa,
kabilar Hebronawa,
kabilar Maliyawa,
kabilar Mushiyawa,
kabilar Korayawa
(Kohat shi ne kakan Amram; 59 sunan matan Amram shi ne Yokebed, ita zuriyar
Lawi ce, wadda aka haifa wa Lawiyawa* a Masar. A wajen Amram kuwa ta
haifi Haruna, Musa da kuma ʼyarʼuwarsu Miriyam. 60 Haruna shi ne mahaifin
Nadab, Abihu, Eleyazar da kuma Itamar. 61 Amma Nadab da Abihu sun mutu
saʼad da suka miƙa hadaya da haramtacciyar wuta a gaban UBANGIJI.)

* **26:59** Ko kuwa Yokebed, ʼyar Lawi, wadda aka haifa wa Lawi

62 Dukan ʼyaʼyan Lawiyawa maza daga wata ɗaya zuwa gaba, jimillarsu ta
kai 23,000. Ba a ƙidaya su tare da sauran Isra'ilawa ba, domin ba a ba su
gādo tare da su ba.

63 Waɗannan su ne waɗanda Musa da Eleyazar firist, suka ƙidaya sa'ad da suka
ƙidaya Isra'ilawa a filaye Mowab kusa da Urdun a hayen Yeriko. 64 Ba ko ɗayansu
da yake cikin waɗanda Musa da Haruna firist, suka ƙidaya sa'ad da suka ƙidaya
Isra'ilawa a Hamadar Sinai. 65 Gama UBANGIJI ya riga ya gaya wa waɗancan Isra'ilawa
cewa lalle za su mutu a hamada, kuma ba ko ɗayansu da ya rage, sai Kaleb ɗan
Yefunne da Yoshuwa ɗan Nun.

# 27

*ʼYaʼyan Zelofehad mata*

1 ʼYaʼyan nan mata na Zelofehad, ɗan Hefer, ɗan Gileyad, ɗan Makir, ɗan
Manasse, suna cikin kabilan Manasse ɗan Yusuf, suka tafi ƙofar shiga Tentin Sujada.
Sunayensu kuwa su ne Mala, Nowa, Hogla, Milka da kuma Tirza. 2 Da suka tafi ƙofar
shiga Tentin Sujada, sai suka tsaya a gaban Musa, Eleyazar firist, shugabannin da
sauran taro, suka ce, 3 "Mahaifinmu ya mutu a hamada. Ba ya cikin mabiyan Kora
waɗanda suka taru suka tayar wa UBANGIJI, amma ya mutu ne saboda zunubinsa,
bai kuma bar ʼyaʼya maza ba. 4 Me ya sa sunan mahaifinmu zai ɓace a kabilarsa don
kawai ba shi da ɗa? Ka ba mu gādo cikin ʼyanʼuwan mahaifinmu."
5 Saboda haka Musa ya kawo maganarsu a gaban UBANGIJI. 6 UBANGIJI kuwa ya ce
wa masa, 7 "Abin da ʼyaʼyan nan mata na Zelofehad suke faɗi gaskiya ne. Dole ka ba
su mallaka a matsayin gādo cikin ʼyanʼuwan mahaifinsu, ka kuma mayar musu da
gādon mahaifinsu.
8 "Ka faɗa wa Isra'ilawa cewa, 'In wani ya mutu ba shi da ɗa, a ba da gādonsa ga
ʼyarsa. 9 In ba shi da diya, sai a ba wa ʼyanʼuwansa gādonsa. 10 In ba shi da ʼyanʼuwa,
a ba da gādonsa ga ʼyanʼuwan mahaifinsa. 11 In mahaifinsa ba shi da ʼyanʼuwa, a
ba da gādonsa ga danginsa na kusa, a kabilarsa don yǎ mallaka. Wannan ya zama
ƙa'ida wa Isra'ilawa, yadda UBANGIJI ya umarci Musa.' "

*Yoshuwa zai gāji Musa*
*(Maimaitawar Shari'a 31.1-8)*

12 Sa'an nan UBANGIJI ya ce wa Musa, "Hau bisa wannan dutse a Abarim. Ka ga
ƙasar da na ba wa Isra'ilawa. 13 Bayan ka gani, kai ma za ka bi ƙafafun mutanenka,
kamar yadda ɗanʼuwanka Haruna ya yi, 14 gama sa'ad da jama'a suka yi tayarwa
saboda rashin ruwa a Hamadan Zin, ku biyu, ba ku kiyaye umarnina don ku ɗaukaka
ni matsayin mai tsarki, a gabansu ba." (Waɗannan su ne ruwaye na Meriba da
Kadesh, a Hamadan Zin.)
15 Musa ya ce wa UBANGIJI, 16 "Bari UBANGIJI, Allah na ruhohin ʼyan adam, yǎ naɗa
wani a kan wannan jama'a 17 yǎ shiga, yǎ kuma fita a gabansu, wanda zai bishe su
zuwa waje, yǎ kuma dawo da su ciki, don kada mutanen UBANGIJI su zama kamar
tumakin da ba su da makiyayi."
18 Sai UBANGIJI ya ce wa Musa, "Ka ɗauki Yoshuwa ɗan Nun, mutumin da ruhun
shugabanci yake a cikinsa, ka ɗibiya masa hannunka. 19 Ka sa yǎ tsaya a gaban
Eleyazar firist, da gaban dukan jama'a, sa'an nan ka keɓe shi a gabansu. 20 Ka danƙa
masa ikonka don dukan jama'a Isra'ilawa su yi masa biyayya. 21 Zai tsaya a gaban
Eleyazar firist, wanda zai nemi masa shawara ta wurin Urim a gaban UBANGIJI. Da
umarninsa, da shi da dukan jama'ar Isra'ilawa za su fita, da umarninsa kuma za su
shiga."

22 Musa ya yi yadda Ubangiji ya umarce shi. Ya ɗauki Yoshuwa, ya sa ya tsaya
a gaban Eleyazar firist, da kuma gaban dukan jama'a. 23 Sai ya ɗibiya masa
hannuwansa, ya keɓe shi, yadda Ubangiji ya umarta ta wurin Musa.

# 28

*Hadayu na kullayaumi*
*(Fitowa 29.38-43; Firistoci 6.8-13)*
1 Sai Ubangiji ya ce wa Musa, 2 "Ka umarci Isra'ilawa cewa, 'Ku tabbatar kun miƙa
mini hadaya ta abinci ta wuta mai daɗin ƙanshi a gare ni, a daidai lokaci.' 3 Ka gaya
musu, 'Ga hadaya ta ƙonawa ta kowace rana, da za ku miƙa wa Ubangiji, raguna
biyu, bana ɗaya-ɗaya, marasa lahani. 4 A miƙa rago ɗaya da safe, ɗaya kuma da
yamma, 5 tare da hadaya ta lallausan gari kashi ɗaya bisa goma na efan, kwaɓaɓɓe
da kwalaba ɗaya na man zaitun mafi kyau. 6 Wannan ita ce hadaya ta ƙonawa ta
kullum wadda aka kafa a Dutsen Sinai, don daɗin ƙanshi, wato, hadaya ce da aka
ƙone da wuta ga Ubangiji. 7 Hadaya ta sha, za tă zama kwalaba ɗaya na ruwan
inabi, da ɗan rago guda. Za a kwarara hadaya ta sha ga Ubangiji a wuri mai tsarki.
8 Ɗayan ɗan ragon kuma za a miƙa shi da yamma, tare irin hadaya ta lallausan gari,
da hadaya ta sha da ka yi da safe. Wannan hadaya ce ta ƙonawa mai daɗin ƙanshi
ga Ubangiji.

*Hadayun Asabbaci*
9 " 'A ranar Asabbaci, za a miƙa 'yan raguna biyu, bana ɗaya-ɗaya marasa lahani,
tare da hadaya ta sha, da hadaya ta lallausan gari kashi biyu bisa goma na efa,
kwaɓaɓɓe da mai. 10 Wannan ita ce hadaya ta ƙonawa ta kowace Asabbaci, ban
da hadaya ta ƙonawa ta kullum, tare da ta hadaya ta sha.

*Hadayu na Kowane Wata*
11 " 'A rana ta fari ga kowane wata, za a miƙa wa Ubangiji hadayun 'yan bijimai
biyu, rago ɗaya, da 'yan tumaki bakwai, bana ɗaya-ɗaya, dukansu kuma marasa
lahani. 12 Da kowane bijimi, a kasance da hadaya ta lallausan garin da aka kwaɓa
da mai na kashi uku bisa goma na efa; da ɗan rago kuwa, a kasance da hadaya ta
lallausan garin da aka kwaɓa da mai na kashi biyu bisa goma na efa; 13 da kowane
tunkiya kuma, a kasance da hadaya ta lallausan garin da aka kwaɓa da mai, na kashi
ɗaya bisa goma na efa. Wannan hadaya ce da aka ƙone da wuta ga Ubangiji. 14 Da
kowane bijimi, za a kasance da hadaya ta sha, na rabin kwalabar ruwan inabi; da
rago kuwa, a kasance da kashi ɗaya bisa uku; da kowace tunkiya kuma, a kasance
da kashi ɗaya bisa huɗu. Wannan ita ce hadaya ta ƙonawa don tsayawar kowane
sabon wata na shekara. 15 Ban da hadaya ta ƙonawa ta kullum tare da hadaya ta sha,
za a miƙa bunsuru ɗaya ga Ubangiji, hadaya ce don zunubi.

*Bikin Ketarewa*
*(Firistoci 23.4-8)*
16 " 'Za a yi Bikin Ketarewa ga Ubangiji a rana ta goma sha huɗu ga wata na fari.
17 A rana ta goma sha biyar ga wannan wata, za a yi biki; kwana bakwai za a ci
burodi marar yisti. 18 A rana ta farko, za ku yi tsattsarkan taro, ba kuwa za a yi
aikin da aka saba yi na kullum ba. 19 Za a miƙa hadaya ta ƙonawa da bijimai biyu,
rago ɗaya, da 'yan raguna bakwai, bana ɗaya-ɗaya; dukansu kuma marasa lahani
ga Ubangiji. 20 Da kowane bijimi, a shirya kashi ɗaya bisa uku na efan lallausan
gari, kwaɓaɓɓe da mai; da rago guda kuwa, a shirya kashi biyu bisa goma na efan
lallausan gari, kwaɓaɓɓe da mai; 21 da kowane 'yan raguna bakwai, kashi ɗaya bisa
goma. 22 A haɗa da bunsuru guda, a matsayin hadaya don zunubi, don yin muku

kafara. 23 Ku shirya wannan tare da hadaya ta ƙonawa ta kowace safiya. 24 Ta haka
za a shirya abinci don hadayar da aka yi da wuta, kowace rana, har kwana bakwai
don daɗin ƙanshi ga UBANGIJI; a shirya shi haɗe da hadaya ta ƙonawa ta kullum, da
kuma hadaya ta sha. 25 A rana ta bakwai, za ku yi tsattsarkan taro, amma ba za a yi
aikin da aka saba yi kullum ba.

*Bikin Makoni*
*(Firistoci 23.15-22)*
26 " 'A ranar nunan fari, sa'ad da za ku miƙa wa UBANGIJI hadayar sabon hatsi, a
lokacin Bikin Makoni, za a yi tsattsarkan taro, ba kuwa za a yi aikin da aka saba yi ba.
27 A miƙa hadaya ta ƙonawa da 'yan bijimai biyu, rago ɗaya da 'yan raguna bakwai,
bana ɗaya-ɗaya don daɗin ƙanshi ga UBANGIJI. 28 Da kowane bijimi a kasance da
hadaya ta lallausan gari kashi uku bisa goma na efa, kwaɓaɓɓe da mai; da rago kuwa,
a kasance da hadaya ta lallausan gari kashi biyu bisa goma na efa, kwaɓaɓɓe da mai;
29 da kowane 'yan raguna bakwai, kashi ɗaya bisa goma. 30 A haɗa da bunsuru guda
don yin muku kafara. 31 A miƙa waɗannan tare da hadayarsu ta sha, haɗe da hadaya
ta ƙonawa ta kullum, da kuma hadayarta ta sha. A tabbata dabbobin nan marasa
lahani ne.

## 29

*Bikin Kahoni*
*(Firistoci 23.23-25)*
1 " 'A rana ta farko ga wata na bakwai, a yi tsattsarkan taro, kada kuma a yi aikin
da aka saba na kullum. Rana ce don busa ƙahoni. 2 Za a miƙa hadaya ta ƙonawa da
bijimi guda, rago guda, 'yan raguna bakwai, bana ɗaya-ɗaya don daɗin ƙanshi ga
UBANGIJI, duka su kasance marasa lahani. 3 Tare da bijimin za a kuma miƙa hadaya
ta gari na kashi ɗaya bisa goma na efa na lallausan gari, kwaɓaɓɓe da mai; da rago
guda, kashi biyu bisa goma na efa na lallausan gari, kwaɓaɓɓe da mai; 4 kowane
'yan raguna bakwai, kashi ɗaya bisa goma. 5 A haɗa da bunsuru guda a matsayin
hadaya don zunubi, don yin muku kafara. 6 Waɗannan ƙari ne ga hadayun ƙonawa
na wata-wata da na kullayaumi, tare da hadayun garinsu da hadayun sha yadda aka
tsara. Hadayu ne da aka miƙa wa UBANGIJI ta wuta don daɗin ƙanshi.

*Ranar Kafara*
*(Firistoci 23.26-32)*
7 " 'A rana ta goma ga wannan watan bakwai, za a yi tsattsarkan taro. Ba za ku ci
abinci ba, ba kuma za ku yi aiki ba. 8 Za a miƙa hadaya ta ƙonawa da bijimi guda, rago
guda, da kuma 'yan raguna bakwai, 'yan bana ɗaya-ɗaya, dukansu marasa lahani
don daɗin ƙanshi ga UBANGIJI. 9 Tare da bijimin a miƙa hadaya ta gari na kashi ɗaya
bisa goma na efa, na lallausan gari kwaɓaɓɓe, da mai; da rago guda, kashi biyu bisa
goma na efa, na lallausan gari kwaɓaɓɓe, da mai; 10 kowane 'yan raguna bakwai,
kashi ɗaya bisa goma. 11 A haɗa da bunsuru guda a matsayin hadaya don zunubi,
don yin muku kafara da kuma hadaya ta ƙonawa ta kullum; tare da hadaya ta garinta,
da kuma hadayu na shansu.

*Bikin tabanakul*
*(Firistoci 23.33-44)*
12 " 'A rana ta goma sha biyar ga wata na bakwai, za a yi tsattsarkan taro, ba kuwa
za a yi aikin da aka saba yi ba. Ku yi biki ga UBANGIJI har kwana bakwai. 13 A
miƙa hadayar da aka yi da wuta, mai daɗin ƙanshi ga UBANGIJI, hadaya ta ƙonawa ta
bijimai guda sha uku, raguna biyu, da 'yan raguna goma sha huɗu, bana ɗaya-ɗaya,
dukansu marasa lahani. 14 Da kowane bijimai goma sha uku nan, a miƙa hadaya ta

gari, kashi uku bisa goma na efa, kwaɓaɓɓe da mai; da ragunan biyu ɗin, a miƙa
hadaya ta gari kashi biyu bisa goma na efa, kwaɓaɓɓe da mai; 15 tare kuma da kowane
ʼyan raguna goma sha huɗu, kashi ɗaya bisa goma. 16 A haɗa da bunsuru guda, a
matsayin hadaya don zunubi, ban da hadaya ta ƙonawa na kullum tare da hadayarta,
ta gari da kuma hadaya ta sha.

17 " 'A rana ta biyu, a miƙa bijimai goma sha biyu, raguna biyu, da ʼyan raguna goma
sha huɗu, bana ɗaya-ɗaya, dukansu marasa lahani. 18 Tare da bijiman, ragunan da
ʼyan ragunan a miƙa hadayarsu da gari da hadaya ta sha, bisa ga adadin da aka
ƙayyade. 19 A haɗa da bunsuru guda a matsayin hadaya, don zunubi, ban da hadaya
ta ƙonawa ta kullum, tare da hadayarta ta gari da hadayunsu ta sha.

20 " 'A rana ta uku za a miƙa bijimai goma sha ɗaya, raguna biyu, da kuma ʼyan
raguna goma sha huɗu, bana ɗaya-ɗaya, dukansu marasa lahani. 21 Tare da bijiman,
ragunan da ʼyan raguna, a miƙa hadayun gari da hadayun sha, bisa ga adadin da aka
ƙayyade. 22 A haɗa da bunsuru guda a matsayin hadaya don zunubi, ban da hadaya
ta ƙonawa ta kullum, tare da hadayarta ta gari da hadaya ta sha.

23 " 'A rana ta huɗu a miƙa bijimai goma, raguna biyu, da ʼyan raguna goma sha
huɗu, bana ɗaya-ɗaya, dukansu marasa lahani. 24 Tare da bijiman, ragunan da kuma
ʼyan raguna, a miƙa hadayunsu na gari da hadayu na sha bisa ga adadin da aka
ƙayyade. 25 A haɗa da bunsuru guda, a matsayin hadaya don zunubi, ban da hadaya
ta ƙonawa ta kullum, tare da hadayarta ta gari da hadaya ta sha.

26 " 'A rana ta biyar a miƙa bijimai tara, raguna biyu, da ʼyan raguna goma sha
huɗu, bana ɗaya-ɗaya, dukansu marasa lahani. 27 Tare da bijiman, ragunan da
kuma ʼyan ragunan, a miƙa hadayu na gari, da hadayu na sha bisa ga adadin da
aka ƙayyade. 28 A haɗa da bunsuru guda a matsayin hadaya don zunubi, ban da
hadaya ta ƙonawa ta kullum, tare da hadayarta ta gari da hadaya ta sha.

29 " 'A rana ta shida a miƙa bijimai takwas, raguna biyu, da ʼyan raguna goma sha
huɗu, bana ɗaya-ɗaya, dukansu marasa lahani. 30 Tare da bijiman, ragunan da kuma
ʼyan raguna, a miƙa hadayunsu ta gari da hadayu na sha bisa adadin da a ƙayyade.
31 A haɗa da bunsuru guda a matsayin hadaya don zunubi, ban da hadaya ta ƙonawa
ta kullum tare da hadayarta ta hatsi da hadaya ta sha.

32 " 'A rana ta bakwai a miƙa bijimai bakwai, raguna biyu da ʼyan raguna goma
sha huɗu, bana ɗaya-ɗaya, dukansu marasa lahani. 33 Tare da bijiman, ragunan da
kuma ʼyan raguna, a miƙa hadayunsu na gari, da hadayun sha bisa ga adadin da a
ƙayyade. 34 A haɗa da bunsuru guda a matsayin hadaya don zunubi, ban da hadaya
ta ƙonawa ta kullum tare da hadayarta ta hatsi da hadayarta ta sha.

35 " 'A rana ta takwas kuwa za a yi tsattsarkan taro, ban da aikin da aka saba. 36 A
miƙa hadayar da aka yi da wuta mai daɗin ƙanshi ga UBANGIJI, a yi hadaya ta ƙonawa
da bijimi guda, rago guda, da ʼyan raguna bakwai, bana ɗaya-ɗaya, dukansu marasa
lahani. 37 Tare da bijimin, ragon da kuma ʼyan ragunan, a miƙa hadayunsu na gari
da hadayu na sha bisa ga adadin da aka ƙayyade. 38 A haɗa da bunsuru guda a
matsayin hadaya don zunubi, ban da hadaya ta ƙonawa ta kullum, tare da hadayarta
ta hatsi da hadayarta ta sha.

39 " 'Ban da abin da kuka yi alkawari, da kuma sadakokinku na yardar rai, a miƙa
waɗannan ga UBANGIJI a lokacin bukukkuwanku, hadayunku na ƙonawa, hadayu na
gari, hadayu na sha da hadayu na salama.' "

40 Musa ya faɗa wa Isra'ilawa dukan abin da UBANGIJI ya umarce shi.

# 30

*Alkawura*

[1] Musa ya ce wa shugabannin kabilan Isra'ila, "Ga abin da UBANGIJI ya umarta.
[2] Sa'ad da mutum ya yi wa UBANGIJI alkawari, ko kuwa ya rantse zai yi wani abu,
kada yă ƙi cika maganarsa, amma yă cika kome da ya faɗa.

[3] "Sa'ad da yarinya, wadda har yanzu tana a gidan mahaifinta ta yi wa UBANGIJI
alkawari, ko ta rantse za tă yi wani abu, [4] mahaifinta kuwa ya ji alkawarin da ta
yi, bai kuma ce mata kome ba, to, sai alkawarin da ta yi da wa'adinta su tabbata.
[5] Amma in mahaifinta ya hana ta, sa'ad da ya ji game da shi, to, ba wani daga cikin
alkawari ko rantsuwar da ta yi zai tabbata; UBANGIJI kuwa zai gafarta mata domin
maihaifinta ya hana ta.

[6] "In ta yi aure, sai daga baya ta yi alkawari ko kuwa leɓunanta sun furta alkawari
da garaje, cewa za tă yi wani abu, [7] mijinta kuwa ya ji game da wannan, amma bai ce
mata kome ba, to, alkawarin da ta yi da kuma rantsuwar da ta yi, su tabbata. [8] Amma
in mijin ya hana ta sa'ad da ya ji, zai warware alkawari da kuma rantsuwar da ta yi
da garaje, UBANGIJI kuwa zai gafarce ta.

[9] "Duk wani alkawari ko rantsuwar da gwauruwa, ko macen da aurenta ya mutu,
ta yi, zai tabbata a kanta.

[10] "In macen aure ta yi alkawari, ko ta rantse za tă yi wani abu, [11] mijinta kuwa
ya ji game da wannan, amma bai ce mata kome ba, bai kuma hana ta ba, to,
dukan alkawari da kuma rantsuwar da ta yi su tabbata a kanta. [12] Amma in mijin
ya warware su sa'ad da ya ji, to, ba wani alkawari ko rantsuwar da ya fito daga
leɓunanta da zai tabbata. Mijinta ya warware su, UBANGIJI kuma zai gafarce ta.
[13] Mijinta yana iya tabbatar, ko yă rushe duk wani alkawari ko rantsuwar da ta ɗauka.
[14] Amma in mijinta bai ce mata kome ba, to, ya tabbatar da dukan alkawarinta da
kuma rantsuwarta ke nan. Ya tabbatar da su ta wurin yin shiru sa'ad da ya ji ta.
[15] Amma in ya ji, sa'an nan daga baya ya hana ta, to, zai sha hukuncin laifinta."

[16] Waɗannan su ne ƙa'idodin da UBANGIJI ya ba wa Musa game da dangantakar miji
da matarsa, da kuma tsakanin mahaifi da 'yarsa wadda har yanzu tana a gidansa.

# 31

*Ɗaukar Fansa a kan Midiyawa*

[1] UBANGIJI ya ce wa Musa, [2] "Ka ɗaukar wa Isra'ilawa fansa, a kan Midiyawa. Bayan
wannan za ka mutu, a kuwa tara ka ga mutanenka."

[3] Saboda haka Musa ya ce wa mutane, "Ku shirya waɗansu daga cikin mazanku,
su tafi su yi yaƙi da Midiyawa don su ɗaukar wa UBANGIJI fansa a kansu." [4] Ku aiki
maza dubu ɗaya daga kowace kabilar Isra'ila. [5] Saboda haka aka samo mayaƙa dubu
goma sha biyu shiryayyu don yaƙi, maza dubu ɗaya daga kowace kabilar Isra'ila.
[6] Musa ya aike su zuwa yaƙi, dubu ɗaya daga kowace kabila, tare da Finehas ɗan
Eleyazar, firist, wanda ya ɗauki kayayyaki daga wuri mai tsarki da ƙahoni don kiran
yaƙi.

[7] Suka yi yaƙi da Midiyawa, suka kashe kowane mutum yadda UBANGIJI ya umarci
Musa. [8] A cikin waɗanda aka kashe kuwa akwai Ewi, Rekem, Zur, Hur da Reba;
sarakuna biyar na Mediyawa. Suka kuma kashe Bala'am ɗan Beyor da takobi.
[9] Isra'ilawa suka kwashe mata da yaran Midiyawa, a matsayin bayi. Suka kwashe
shanunsu da tumakinsu da kuma dukan dukiyarsu, a matsayin ganima. [10] Suka ƙone
dukan garuruwan da Midiyawa suke zama, da dukan sansaninsu. [11] Suka kwashe
dukan ganima haɗe da mutane da dabbobi, [12] suka kawo bayi da ganiman nan, wurin
Musa da Eleyazar firist, da kuma jama'ar Isra'ilawa, a sansaninsu a filayen Mowab
kusa da Urdun daga ƙetaren Yeriko.

[13] Musa, da Eleyazar firist da dukan shugabannin jama'a, suka fito suka tarye su a
bayan sansani. [14] Musa kuwa ya husata da shugabannin sojojin da suke shugabannin
dubbai da shugabannin ɗari-ɗarin da suka dawo daga yaƙi.
[15] Ya tambaye su ya ce, "Kun bar dukan mata da rai? [16] Su ne waɗanda suka bi
shawarar Bala'am suka kuma zama sanadin sa Isra'ilawa suka juya wa UBANGIJI baya,
har ya kawo abin da ya faru da Feyor, har annoba ya kashe dukan mutanen UBANGIJI.
[17] Yanzu ku kashe dukan yara maza, ku kuma kashe kowace macen da ta yi lalata da
namiji, [18] amma ku bar kowace yarinyar da ba tă taɓa yin lalata da namiji ba.
[19] "Dukanku da kuka kashe mutum, ko kuka taɓa wani da aka kashe, dole ku
kasance a bayan sansani har kwana bakwai. A rana ta uku da rana ta bakwai dole
ku tsabtacce kanku da kuma bayinku. [20] Ku tsarkake kowace taguwa da kuma kome
da aka yi da fata, da gashin akuya, ko kuwa itace."
[21] Sa'an nan Eleyazar firist, ya ce wa sojojin da suka je yaƙi, "Wannan ita ce ƙa'idar
da UBANGIJI ya ba wa Musa. [22] Zinariya, azurfa, tagulla, baƙin ƙarfe, kuza, darma [23] da
dukan abin da wuta ba ta iya ci, dole yă shiga wuta sa'an nan zai zama da tsabta.
Amma dole a kuma tsarkake ta da ruwan tsarkakewa. Duk abin da wuta za tă iya ci,
dole a shigar da ita a ruwan tsarkakewa. [24] A rana ta bakwai za ku wanke tufafinku,
sa'an nan za ku tsarkaka, bayan haka ku shigo sansani."

### *Rabawa ganima*

[25] UBANGIJI ya yi magana da Musa ya ce, [26] "Da kai da Eleyazar firist, da shugabannin
jama'a, ku ƙidaya dukan mutane da dabbobin da aka ci da yaƙi. [27] Ku kasa ganimar
kashi biyu, ku ba sojojin da suka tafi yaƙi kashi ɗaya, kashi ɗaya kuma ku ba wa
jama'a. [28] Daga sojojin da suka je yaƙin kuwa, ka ware ganima wa UBANGIJI, ka ɗauki
ɗaya daga cikin mutum ɗari biyar, da shanu ɗari biyar, da jakuna ɗari biyar, da
tumaki ɗari biyar. [29] Ka ɗauki wannan sashe daga rabin rabonsu ka ba wa Eleyazar
firist, a matsayin sashe na UBANGIJI. [30] Daga cikin rabin rabon Isra'ilawa, ka zaɓi
ɗaya daga kowane hamsin na mutane, shanu, jakuna, tumaki, awaki ko kuma sauran
dabbobi. Ka ba wa Lawiyawan da suke lura da tabanakul na UBANGIJI." [31] Saboda
haka Musa da Eleyazar suka aikata yadda UBANGIJI ya umarci Musa.
[32] Yawan ganimar da sojoji suka kawo ita ce tumaki 675,000 [33] shanu 72,000 [34] da
jakuna 61,000. [35] Akwai kuma mata 32,000 da ba su yi lalata ba da namiji ba.

[36] Kashin da aka ba sojoji waɗanda suka tafi yaƙi shi ne,

tumaki 337,500, [37] tumakin da aka ware wa UBANGIJI kuwa 657 ne;
[38] shanu 36,000, shanun da aka ware wa UBANGIJI kuwa 72 ne;
[39] jakuna 30,500, jakunan da aka ware wa UBANGIJI kuwa 61 ne;
[40] mutane 16,000, mutanen da aka ware wa UBANGIJI kuwa 32 ne.

[41] Musa ya ba wa Eleyazar abin da aka ware wa UBANGIJI, kamar yadda UBANGIJI
ya umarci Musa.
[42] Kashin da aka ba wa Isra'ilawa, wanda Musa ya ware daga cikin na waɗanda
suka tafi yaƙi, [43] kashin da aka ba wa jama'a kuwa tumaki 337,500 ne, [44] shanu 36,000,
[45] jakuna 30,500 [46] da mutane 16,000. [47] Daga rabin kashi na Isra'ilawa, Musa ya ɗauki
ɗaya daga cikin hamsin na mutane da na dabbobi, yadda UBANGIJI ya umarce shi, ya
ba wa Lawiyawan da suke lura da tabanakul na UBANGIJI.
[48] Sai shugabannin da suka shugabancin rundunar yaƙin, shugabanni na dubu-
dubu da shugabanni na ɗari-ɗari, suka zo wurin Musa [49] suka ce masa, "Barorinka
sun ƙidaya mayaƙan da suke ƙarƙashinmu, babu ko ɗayan ya ɓace. [50] Saboda

haka mun kawo wa UBANGIJI hadaya na kayan zinariya da kowannenmu ya samu, mundaye, ƙawane, ʼyan kunne da duwatsun wuya, don yin wa kanmu kafara a gaban UBANGIJI."

51 Musa da Eleyazar firist, suka karɓi zinariya da kayan adon duka daga gare su.
52 Dukan zinariya da shugabannin dubu-dubu da shugabannin ɗari-ɗari, waɗanda
Musa da Eleyazar suka karɓa, suka kuma miƙa hadaya ga UBANGIJI, nauyinta ta kai
shekel 16,750. 53 Kowane soja, ya kwashi ganima wa kansa. 54 Musa da Eleyazar
firist, suka karɓi zinariya daga shugabannin dubu-dubu da shugabannin ɗari-ɗari,
suka kawo cikin Tentin Sujada, don su zama abin tuni ga Isra'ilawa a gaban UBANGIJI.

# 32

*Kabilan hayen Urdun*
*(Maimaitawar Shari'a 3.12-22)*

1 Mutanen Ruben da mutanen Gad, da suke da garken shanu da kuma garke
tumaki masu yawa, suka ga cewa ƙasashen Yazer da Gileyad wurare ne masu kyau
don kiwon shanu da tumaki. 2 Saboda haka suka zo wurin Musa da Eleyazar da
kuma shugabannin jama'a, suka ce, 3 "Atarot, Dibon, Yazer, Nimra, Heshbon, Eleyale,
Sebam, Nebo da Beyon, 4 ƙasar da UBANGIJI ya ci da yaƙi a gaban mutane Isra'ila,
suna da kyau don dabbobi, bayinku kuma suna da dabbobi." 5 Suka ce, "In mun sami
tagomashi daga gare ka bari a ba da wannan ƙasa ga bayinka, tă zama mallakanmu.
Kada ka sa mu haye Urdun."

6 Musa ya ce wa mutanen Gad da mutanen Ruben, "Wato, sai ʼyanʼuwanku su yi ta
yaƙi ku kuwa ku zauna nan? 7 Don me za ku karya zuciya Isra'ilawa daga hayewa
zuwa ƙasar da UBANGIJI ya ba su? 8 Haka iyayenku suka yi sa'ad da na aike su daga
Kadesh Barneya don su dubo ƙasar. 9 Gama bayan suka haura Kwarin Eshkol suka
hangi ƙasar, sai suka karya zuciyar Isra'ilawa daga shigar ƙasar da UBANGIJI ya ba su.
10 A ranar kuwa UBANGIJI ya husata har ya yi wannan rantsuwa cewa, 11 'Tabbatacce
ba wani daga cikin mutanen da suka fito daga Masar, tun daga mai shekara ashirin
zuwa gaba, da zai ga ƙasar da na rantse zan ba Ibrahim, da Ishaku, da Yaƙub, domin
ba su bi ni sosai ba, 12 ba ko ɗaya sai dai Kaleb ɗan Yefunne Bakenizze da Yoshuwa
ɗan Nun, don su ne kaɗai suka bi UBANGIJI da zuciya ɗaya.' 13 UBANGIJI ya husata da
Isra'ila har ya sa suka yi ta yawo a hamada shekara arba'in, sai da dukan tsaran da
suka aikata wannan mugunta a gabansa, suka mutu.

14 "Ga shi ku kuma, tarin masu zunubi, kuna tsaya a matsayin kakanninku, kuna sa
UBANGIJI yă sāke husata da Isra'ila. 15 In kun juye daga binsa, zai sāke barin dukan
wannan mutane a hamada, ku ne kuwa za ku zama sanadin hallakarsu."

16 Sai suka zo wurin Musa, suka ce, "Muna so mu gina katangar dutse don
dabbobinmu, da kuma birane don matanmu da ʼyaʼyanmu a nan. 17 Matanmu da
ʼyaʼyanmu za su zauna a biranen da suke da katanga, don kāriya daga mazaunan
ƙasar, amma mu, za mu ɗauki makamai mu tafi tare da sauran Isra'ilawa, har mu
kai su wuraren zamansu. 18 Ba za mu koma gidajenmu ba sai kowane mutumin
Isra'ila ya sami gādonsa. 19 Ba za mu ci gādo tare da su a wancan hayin Urdun ba,
domin mun sami gādonmu a wannan hayin gabashin Urdun."

20 Sai Musa ya ce musu, "In za ku yi haka, in za ku sha ɗamara da makamai a gaban
UBANGIJI, ku tafi yaƙi, 21 in kuma dukanku za ku yi ɗamara, ku ɗauki makaman yaƙi a
hayin Urdun a gaban UBANGIJI har lokacin da ya kori abokan gābansa daga gabansa,
22 to, sa'ad da aka ci ƙasar a gaban UBANGIJI, kwa kuɓuta daga alhakinku ga UBANGIJI
da kuma Isra'ila. Kasan nan kuwa za tă zama mallakarku a gaban UBANGIJI.

23 “Amma in ba ku yi haka ba, kun yi zunubi ke nan ga UBANGIJI; kuma ku san
cewa zunubinku zai tone ku. 24 Ku gina birane domin matanku da ’ya’yanku, ku gina
katanga kuma domin dabbobinku, amma fa ku cika abin da kuka yi alkawari.”
25 Mutanen Gad da mutanen Ruben, suka ce wa Musa, “Mu bayinka za mu yi yadda
ranka yă daɗe ya umarta. 26 ’Ya’yanmu da matanmu, garkunan shanunmu da na
tumakinmu, za su kasance a nan biranen Gileyad. 27 Amma bayinka, kowane mutum
a cikinmu zai haye a gaban UBANGIJI, zuwa yaƙi kamar yadda ranka yă daɗe ya faɗa.”
28 Sai Musa ya yi wa Eleyazar firist, da Yoshuwa ɗan Nun, da shugabannin gidajen
kakannin kabilan mutanen Isra’ila kashedi a kansu, 29 ya ce, “In kowane sojan
mutanen Gad da na mutanen Ruben, ya ɗauki makaman yaƙi, ya haye Urdun tare
da ku a gaban UBANGIJI, to, sa’ad da a ci ƙasar a gabanku, ku ba da ƙasar Gileyad tă
zama mallakarsu. 30 Amma in ba su haye tare da ku da shirin yaƙi ba, to, sai ku ba
su gādo a wancan haye kamar sauran kabilun a Kan’ana.”
31 Mutanen Gad da mutanen Ruben suka amsa, suka ce, “Barorinka za su yi abin da
UBANGIJI ya faɗa. 32 Za mu haye a gaban UBANGIJI zuwa Kan’ana, amma mallakarmu
ta gādo, za tă kasance a wannan hayi na Urdun.”
33 Sai Musa ya ba wa mutanen Gad, mutanen Ruben, da rabin mutanen Manasse
ɗan Yusuf, masarautar Sihon, sarkin Amoriyawa, da masarautar Og na Bashan,
dukan ƙasar, tare da biranenta da kuma yankunan da suke kewaye.
34 Mutanen Gad suka gina Dibon, Atarot, Arower, 35 Atrot Shofan, Yazer, Yogbeha,
36 Bet-Nimra, da Bet-Haran a matsayin birane masu katanga, suka kuma gina katanga
don dabbobinsu. 37 Mutanen Ruben suka sāke gina Heshbon, Eleyale, da Kiriyatayim,
38 haka kuma suka gina Nebo da Ba’al-Meyon (an canja waɗannan sunaye) suka kuma
gina Sibma. Suka ba wa biranen da suka sāke ginawa sunaye. 39 Zuriyar Makir ɗan
Manasse suka tafi Gileyad, suka ci ta da yaƙi, suka kori mutanen Amoriyawa da suke
can.
40 Saboda haka Musa ya ba da Gileyad ga mutanen Makir, zuriyar Manasse, suka
kuma zauna a can. 41 Yayir, wani ɗan Manasse, ya ci ƙauyukansu da yaƙi, ya kuma
ba su sunan Hawwot Yayir. 42 Noba kuma ya ci Kenat da ƙauyukanta da yaƙi, ya
kuma ba ta suna Noba, bisa ga sunansa.

# 33

*Wurare a tafiye-tafiyen Isra’ila*

1 Ga wuraren da Isra’ilawa suka yi sansani sa’ad da suka fito runduna-runduna a
ƙarƙashin Musa da Haruna daga Masar. 2 Bisa ga umarnin UBANGIJI, Musa ya rubuta
wuraren tafiye-tafiyensu da sansaninsu. Ga yadda tafiye-tafiyen suka kasance.

3 Isra’ilawa sun tashi daga Rameses a rana ta goma sha biyar, ga watan
fari, kashegarin Bikin Ketarewa. Suka fita gabagadi a gaban dukan Masarawa,
4 waɗanda suke binne gawawwakin ’ya’yan farinsu da UBANGIJI ya karkashe; gama
UBANGIJI ya hukunta allolinsu.

5 Isra’ilawa suka tashi daga Rameses, suka yi sansani a Sukkot.

6 Suka tashi daga Sukkot, suka yi sansani a Etam, a gefen hamada.

7 Suka tashi daga Etam, suka koma baya zuwa Fi Hahirot, wajen gabashin Ba’al-
Zafon, suka yi sansani kusa da Migdol.

8 Suka tashi daga Fi Hahirot, suka ratsa cikin teku zuwa hamada, bayan sun yi
tafiya kwana uku a cikin Hamadan Etam, sai suka yi sansani a Mara.

9 Suka tashi daga Mara, suka tafi Elim, inda akwai maɓulɓulan ruwa goma sha
biyu, da itatuwan dabino guda saba’in, suka yi sansani a can.

10 Suka tashi daga Elim, suka yi sansani kusa da Jan Teku.

11 Suka tashi daga Jan Teku, suka yi sansani a Hamadan Sin.
12 Suka tashi daga Hamadan Sin, suka yi sansani a Dofka.
13 Suka tashi daga Dofka, suka yi sansani a Alush.
14 Suka tashi daga Alush, suka yi sansani a Refidim, inda babu ruwan da mutane za su sha.
15 Suka tashi daga Refidim, suka yi sansani a Hamadan Sinai.
16 Suka tashi daga Hamadan Sinai, suka yi sansani a Kibrot Hatta'awa.
17 Suka tashi daga Kibrot Hatta'awa, suka yi sansani a Hazerot.
18 Suka tashi daga Hazerot, suka yi sansani a Ritma.
19 Suka tashi daga Ritma, suka yi sansani a Rimmon Ferez.
20 Suka tashi daga Rimmon Ferez, suka yi sansani a Libna.
21 Suka tashi daga Libna, suka yi sansani a Rissa.
22 Suka tashi daga Rissa, suka yi sansani a Kehelata.
23 Suka tashi daga Kehelata, suka yi sansani a Dutsen Shefer.
24 Suka tashi daga Dutsen Shefer, suka yi sansani a Harada.
25 Suka tashi daga Harada, suka yi sansani a Makhelot.
26 Suka tashi daga Makhelot, suka yi sansani a Tahat.
27 Suka tashi daga Tahat, suka yi sansani a Tera.
28 Suka tashi daga Tera, suka yi sansani a Mitka.
29 Suka tashi daga Mitka, suka yi sansani a Hashmona.
30 Suka tashi daga Hashmona, suka yi sansani a Moserot.
31 Suka tashi daga Moserot, suka yi sansani a Bene Ya'akan.
32 Suka tashi daga Bene Ya'akan, suka yi sansani a Hor Haggidgad.
33 Suka tashi daga Hor Haggidgad, suka yi sansani a Yotbata.
34 Suka tashi daga Yotbata, suka yi sansani a Abrona.
35 Suka tashi daga Abrona, suka yi sansani a Eziyon Geber.
36 Suka tashi daga Eziyon Geber, suka yi sansani a Kadesh, cikin Hamadan Zin.
37 Suka tashi daga Kadesh, suka yi sansani a Dutsen Hor, a iyakar Edom. 38 Bisa ga
umarni Ubangiji, Haruna firist, ya hau Dutsen Hor, inda ya mutu a rana ta fari ga
watan biyar, a shekara ta arba'in, bayan Isra'ilawa suka fito daga Masar. 39 Haruna
yana da shekara ɗari da ashirin da uku, sa'ad da ya mutu a Dutsen Hor.
40 Sarki Arad Bakan'ane, wanda yake zaune a Negeb na Kan'ana, ya ji labari cewa Isra'ilawa suna zuwa.
41 Suka tashi daga Dutsen Hor, suka yi sansani a Zalmona.
42 Suka tashi daga Zalmona, suka yi sansani a Funon.
43 Suka tashi daga Funon, suka yi sansani a Obot.
44 Suka tashi daga Obot, suka yi sansani a Iye Abarim, a iyakar Mowab.
45 Suka tashi daga Iyim*, suka yi sansani a Dibon Gad.
46 Suka tashi daga Dibon Gad, suka yi sansani a Almon Dibilatayim.
47 Suka tashi daga Almon Dibilatayim, suka yi sansani a duwatsun Abarim, kusa da Nebo.
48 Suka tashi daga duwatsun Abarim, suka yi sansani a filayen Mowab kusa da
Urdun, ɗaura da Yeriko. 49 A can filayen Mowab, suka yi sansani kusa da Urdun
ɗaura da Bet-Yeshimot har zuwa Abel-Shittim.

50 A filayen Mowab kusa da Urdun ɗaura da Yeriko ne Ubangiji ya ce wa Musa,
51 “Ka gaya wa Isra'ilawa cewa, ‘Sa'ad da kuka haye Urdun zuwa Kan'ana, 52 ku kori
dukan mazaunan ƙasar a gabanku. Ku rurrushe sassaƙaƙƙun duwatsu, da siffofinsu
na zubi, ku kuma rurrushe dukan masujadansu na kan tudu. 53 Ku mallaki ƙasar, ku

* **33:45** Wato, Iye Abarim.

kuma zauna a ciki, gama na ba ku ƙasar, ku mallake ta. 54 Ku rarraba ƙasar ta wurin
jefan ƙuri'a, bisa ga kabilanku. Kabilar da take babba, a ba ta babban gādo, ƙarami
kabila kuwa, a ba ta ƙaramin gādo. Duk abin da ƙuri'a ta ba su, shi zai zama nasu.
Ku rarraba wannan bisa zuriyar kakanninku.
55 " 'Amma in ba ku kori mazaunan ƙasar ba, waɗanda kuka bari su ci gaba da
zama, za su zama muku hakki a idanunku, da kuma ƙayayyuwa a bayanku. Za su ba
ku wahala a ƙasar da kuke zama. 56 Sa'an nan kuwa zan yi muku abin da na shirya
yin musu.' "

# 34

*Iyakokin Kan'ana*

1 UBANGIJI ya ce wa Musa, 2 "Ka umarci Isra'ilawa, ka ce musu, 'Sa'ad da
kuka shiga Kan'ana, ƙasar da aka ba ku gādo za tă kasance da waɗannan
iyakoki.

3 " 'Gefenku na kudu zai haɗa da wani sashin Hamadan Zin ta iyakar Edom. A
gabas, iyakarku ta kudu za tă fara daga ƙarshen Tekun Gishiri,* 4 tă ƙetare
Mashigin Kunama† a kudu, tă ci gaba zuwa Zin, sa'an nan tă nufi kudu da Kadesh
Barneya. Sa'an nan za tă zarce zuwa Hazar Addar, tă nausa zuwa Azmon, 5 inda
za tă juya tă haɗu da Rafin Masar, tă kuma ƙarasa a Bahar Rum.‡
6 " 'Iyakarku a yammanci, za tă kasance bakin Bahar Rum. Wannan ce za tă zama
iyakarku a yamma.
7 " 'Iyakarku a arewanci kuwa za tă tashi daga Bahar Rum zuwa Dutsen Hor, 8 za
tă kuma tashi daga Dutsen Hor, zuwa Lebo§ Hamat. Sa'an nan tă miƙe zuwa Zedad,
9 tă ci gaba zuwa Zifron, sa'an nan tă ƙarasa a Hazar-Enan. Wannan ce za tă zama
iyakarku a arewa.
10 " 'Iyakarku a gabashi, za tă tashi daga Hazar-Enan zuwa Shefam. 11 Iyakar za
tă gangara daga Shefam zuwa Ribla a gefen gabashin Ayin, sa'an nan tă ci gaba a
gangaren gabashin Tekun Kinneret.* 12 Sa'an nan tă gangara ta Urdun, tă ƙarasa a
Tekun Gishiri.
" 'Wannan za tă zama ƙasarku, tare da iyakokinta a kowane gefe.' "
13 Sai Musa ya umarci Isra'ilawa ya ce, "Ku raba wannan ƙasa da za ku gāda ta
hanyar jefa ƙuri'a. UBANGIJI ya umarta cewa a ba da ita ga kabilu tara da rabi,
14 saboda iyalan kabilar Ruben, kabilar Gad da rabin kabilar Manasse sun riga sun
sami gādonsu. 15 Waɗannan kabilu biyu da rabi, sun sami gādonsu a wancan hayin
Urdun a gabashin Yeriko† wajen fitowar rana."
16 UBANGIJI ya ce wa Musa, 17 "Waɗannan su ne sunayen mutanen da za su raba
muku ƙasar gādo. Eleyazar firist, da Yoshuwa ɗan Nun. 18 Ka kuma naɗa shugaba
guda ɗaya daga kowace kabila domin yă taimaka a rabon ƙasar.

19 "Ga sunayensu.

"Kaleb ɗan Yefunne, daga kabilar Yahuda;
20 Shemuyel ɗan Ammihud, daga kabilar Simeyon
21 Elidad ɗan Kislon, daga kabilar Benyamin;
22 Bukki ɗan Yogli, shugaba daga kabilar Dan;

* 34:3 Wato, Mataccen Teku; haka ma a aya 12. † 34:4 Da Ibraniyanci Akrabbim ‡ 34:5 Wato, Mediterraniyan; haka kuma a ayoyi 6 da 7. § 34:8 Ko Kuwa zuwa mashigin * 34:11 Wato, Galili † 34:15 Urdun na Yeriko mai yiwuwa tsohuwar suna ce ta Kogin Urdun.

23 Hanniyel ɗan Efod, shugaba daga kabilar Manasse ɗan Yusuf;
24 Kemuwel ɗan Shiftan, shugaba daga kabilar Efraim ɗan Yusuf;
25 Elizafan ɗan Farnak, shugaba daga kabilar Zebulun;
26 Faltiyel ɗan Azzan, shugaba daga kabilar Issakar;
27 Ahihud ɗan Shelomi, shugaba daga kabilar Asher;
28 Fedahel ɗan Ammihud, shugaba daga kabilar Naftali.”

29 Waɗannan su ne mutanen da Ubangiji ya umarta su raba gādo ga
Isra’ilawa a ƙasar Kan’ana.

# 35

*Garuruwan Lawiyawa*

1 A filayen Mowab, wajen Urdun, ɗaura da Yeriko, Ubangiji ya yi magana da Musa
ya ce, 2 “Ka umarci Isra’ilawa su ba wa Lawiyawa garuruwan da za su zauna a ciki
daga cikin gādon da Isra’ilawa za su mallaka. A kuma ba su wurin kiwo kewaye da
garuruwan. 3 Sa’an nan za su kasance da garuruwan da za su zauna, su sami fili, da
kuma za su yi kiwon garkensu na shanu da tumaki da kuma sauran dabbobinsu.
4 “Wuraren kiwo a kewayen garuruwan da za a ba wa Lawiyawa, girmansu zai
zama mai fāɗin kamu dubu ɗaya daga katangar garin. 5 A bayan garin, ka auna
kamu dubu biyu a wajen gabas, kamu dubu biyu a wajen yamma, kamu dubu biyu
wajen kudu, da kuma kamu dubu uku wajen arewa, a bar garin a tsakiya. Za su
kasance da wannan a matsayin wurin kiwo na garuruwan.

*Biranen mafaka*

6 “A cikin biranen da za a ba Lawiyawa, shida daga cikin garuruwan za su zama
biranen mafaka, inda wanda ya kashe mutum zai gudu yǎ je. Ban da wannan, a ba
su waɗansu garuruwa arba’in da biyu. 7 Duka-duka dai a ba Lawiyawa garuruwa
arba’in da takwas, tare da wuraren kiwonsu. 8 Garuruwan da za ku ba wa Lawiyawa
daga ƙasar da Isra’ilawa suka mallaka, za a ba da su bisa girman gādon kowace
kabila. Ka karɓi garuruwa masu yawa daga kabilar da take da garuruwa masu yawa,
amma kaɗan daga kabilar da ba ta da garuruwa masu yawa.”

*(Maimaitawar Shari’a 19.1-13; Yoshuwa 20.1-9)*

9 Sa’an nan Ubangiji ya ce wa Musa, 10 “Ka yi magana da Isra’ilawa, ka ce musu,
‘Sa’ad da kuka haye Urdun zuwa Kan’ana, 11 ku zaɓi waɗansu garuruwan da za su
zama biranen mafakarku, inda wanda ya kashe mutum cikin kuskure zai iya gudu
zuwa. 12 Za su zama wuraren mafaka daga hannun mai bin hakki, don kada a kashe
mai kisankai, tun ba a kai shi gaban shari’a, a gaban taron jama’a ba. 13 Waɗannan
garuruwa shida da aka bayar za su zama biranen mafakarku. 14 A ba da uku a
wannan gefe na Urdun, a kuma ba da uku a Kan’ana, su zama biranen mafaka.
15 Waɗannan garuruwa shida za su zama wurin mafaka wa Isra’ilawa, baƙi da duk
sauran mutanen da suke zama a cikinsu, saboda duk wanda ya kashe mutum cikin
kuskure yǎ iya gudu zuwa.
16 “ ‘In wani ya bugi wani da makami na ƙarfe har ya mutu, to, shi mai kisankai
ne; sai a kashe mai kisankan nan. 17 Ko kuwa in wani yana riƙe da dutsen da ya
isa yǎ kashe mutum a hannunsa, ya kuma harbi wani da dutsen har ya mutu, to, shi
mai kisankai ne, sai a kashe mai kisankan nan. 18 Ko kuwa wani yana da makami na
itace a hannunsa da ya isa yǎ kashe mutum, ya kuma bugi wani da shi har ya mutu,
shi ma mai kisankai ne, sai a kashe mai kisankan nan. 19 Sai mai bin hakkin jinin yǎ
kashe mai kisankan, sa’ad da ya sadu da mai kisankan, sai yǎ kashe shi. 20 In saboda
ƙiyayya, mutum ya laɓe, ya soke wani, ko ya jefe shi da wani abu da gangan har ya

mutu, 21 ko kuwa saboda ƙiyayya ya naushe shi har ya mutu, sai a kashe wannan
mutumin da ya yi haka; shi mai kisankai ne. Sai mai bin hakkin jini yă kashe mai
kisankan in ya same shi.

22 " 'Amma in cikin tsautsayi ne ya soke shi, ba don ƙiyayya ba, ko kuma ya jefe shi,
ba da gangan ba, 23 ko kuwa bai gan shi ba, ya jefa dutsen da zai kashe shi a kansa, ya
kuwa mutu, to, da yake shi ba abokin gābansa ba ne, bai kuma yi nufi yă ji masa ba,
24 dole taro su yi hukunci tsakanin mai laifin, da mai bin hakkin jini bisa waɗannan
ƙa'idodi. 25 Dole taro su kāre wanda ake zargi da kisa, daga mai bin hakkin jini. Su
mai da shi birnin mafaka inda ya gudu ya tafi. Dole yă kasance a can sai mutuwar
babban firist, wanda aka shafe da mai mai tsarki.

26 " 'Amma in wanda ake zargin ya kuskura ya fita, ya kai iyakar birnin mafaka
wadda ya gudu ya je, 27 idan mai bin hakkin jinin ya same shi a bayan gari, mai bin
hakkin jinin zai iya kashe mai kisankai ɗin ba tare da wani laifi ba. 28 Dole wanda
ake zargin, yă kasance a birninsa na mafaka sai bayan mutuwa babban firist; sai
bayan mutuwar babban firist ne kawai zai iya komo ga mallakarsa.

29 " 'Waɗannan su ne za su zama ƙa'idodin da za ku kasance da su, a dukan
tsararraki masu zuwa.

30 " 'Kowa da ya kashe wani, za a kashe shi a matsayin mai kisankai, bisa ga shaidar
shaidu. Amma kada a kashe wani bisa ga shaidar mutum ɗaya.

31 " 'Kada a karɓi fansa don ran wanda ya yi kisankai, wanda ya cancanci mutuwa.
Lalle ne a kashe shi.

32 " 'Kada a karɓi fansa saboda wanda ya tsere zuwa birnin mafaka don yă koma
yă zauna gidansa tun babban firist bai rasu ba.

33 " 'Kada ku ƙazantar da ƙasar da kuke zama a ciki. Zub da jini yakan ƙazantar
da ƙasa, ba a kuma iya yin kafara saboda wannan ƙasa da aka zub da jini, sai dai ta
wurin jinin mutumin da ya zub da jinin. 34 Kada ku ƙazantar da ƙasar da kuke zama,
wadda ni kuma nake zama a ciki, gama Ni UBANGIJI, ina zama a cikin Isra'ilawa.' "

# 36

*Gādon 'ya'yan Zelofehad mata*

1 Sai shugabannin gidajen iyalan Gileyad ɗan Makir, ɗan Manasse, waɗanda suka
fito daga kabilar zuriyar Yusuf, suka zo, suka yi magana a gaban Musa da shugabanni,
shugabannin iyalan Isra'ilawa. 2 Suka ce, "Sa'ad da UBANGIJI ya umarce ranka yă
daɗe, yă raba ƙasar gādo ga Isra'ilawa ta wurin ƙuri'a, ya umarce ka, ka ba wa 'ya'ya
matan nan na Zelofehad ɗan'uwanmu gādonsa. 3 To, a ce sun auri mutane daga
waɗansu kabilan Isra'ilawa fa; ka ga, za a ɗebe gādonsu daga gādon kakanninmu a
ƙara wa gādon kabilan mutanen da suka aura ke nan. Ta haka za a ɗebe sashe daga
gādon da aka ba mu ke nan. 4 Sa'ad da Shekara ta Murnar Isra'ilawa ta kewayo, za
a haɗa gādonsu da na kabilan mutanen da suka aura, a kuma ba su mallakar gādon
da aka ɗebe daga kabilar kakanninmu."

5 Ta wurin umarnin UBANGIJI, Musa ya ba Isra'ilawa wannan umarni, "Abin da
kabilar zuriyar Yusuf suke faɗi, daidai ne. 6 Ga abin da UBANGIJI ya umarta saboda
'ya'ya matan nan na Zelofehad. Za su iya auri duk wanda suka ga dama, muddin sun
yi aure a cikin kabilar kakanninsu. 7 Ba gādon Isra'ilan da za a ba wa wata kabila
daga wata kabila, gama kowane mutumin Isra'ila zai riƙe gādonsa na kabilar da ya
gāda daga kakanninsa. 8 Kowace 'ya wadda ta ci gādon ƙasa, a kowace kabilar
Isra'ilawa, dole tă auri wani cikin kabilar kakanninta, saboda kowane mutumin
Isra'ila yă mallaki gādon kakanninsa. 9 Ba gādon da za a ba wa wata kabila daga
wata kabila, gama kowace kabilar Isra'ilawa za tă riƙe mallaka da ta gāda."

10 Saboda haka ʼyaʼyan Zelofehad mata suka yi yadda UBANGIJI ya umarci Musa.
11 ʼYaʼyan Zelofehad mata, Mala, Tirza, Hogla, Milka da Nowa, suka auri ʼyaʼyan
ʼyanʼuwa na gefen mahaifinsu. 12 Suka yi aure cikin kabilar zuriyar Manasse ɗan
Yusuf, gādonsu kuwa ya kasance a cikin iyali da kuma kabilar mahaifinsu.

13 Waɗannan su ne umarnai da ƙaʼidodin da UBANGIJI ya ba wa Israʼilawa ta wurin Musa, a filayen Mowab kusa da Urdun, ɗaura da Yeriko.

# Maimaitawar Shari'a

*Umarni a bar Horeb*

1 Waɗannan su ne kalmomin da Musa ya yi wa dukan Isra'ila, a hamada gabas
da Urdun, wato, Araba, ɗaura da Suf, tsakanin Faran da Tofel, Laban, Hazerot da
Dizahab. 2 (Yakan ɗauki kwana goma sha ɗaya daga Horeb zuwa Kadesh Barneya ta
hanyar Dutsen Seyir.)

3 A shekara ta arba'in, a rana ta fari ga wata na goma sha ɗaya, Musa ya yi shela
ga Isra'ilawa game da dukan abin da UBANGIJI ya umarta shi game da su. 4 Wannan
ya faru bayan ya ci Sihon sarkin Amoriyawa wanda ya yi mulki a Heshbon da yaƙi.
A Edireyi kuma ya ci Og sarkin Bashan wanda ya yi mulki a Ashtarot da yaƙi.

5 Gabas da iyakar Mowab, Musa ya fara bayyana wannan doka, yana cewa,

6 UBANGIJI Allahnmu ya faɗa mana a Horeb cewa, "Daɗewarku a wannan dutse ya
isa haka. 7 Ku tashi, ku ci gaba zuwa ƙasar tudun Amoriyawa; ku tafi wurin dukan
maƙwabta a cikin Araba, a cikin duwatsu, a gindin yammancin tuddai, a Negeb da
kuma a ta kwaruruka, da ƙasar Kan'aniyawa da kuma zuwa Lebanon, har zuwa
babban kogi, wato, Yuferites. 8 Duba na riga na ba ku wannan ƙasa. Ku shiga ku
mallaki ƙasar da UBANGIJI ya rantse zai ba wa kakanninku, ga Ibrahim, Ishaku da
kuma Yaƙub, da kuma ga zuriyarsu bayansu."

*Naɗin shugabanni*
*(Fitowa 18.13-27)*

9 A wancan lokaci na faɗa muku cewa, "Ku kaya ne masu nauyi da ni kaɗai ba
zan iya ɗauka ba. 10 UBANGIJI Allahnku ya ƙara yawanku har yau kuka zama da
yawa kamar taurari a sarari. 11 Bari UBANGIJI, Allahn kakanninku yă ƙara yawanku
sau dubu, yă kuma albarkace ku yadda ya yi alkawari! 12 Amma yaya zan ɗauka
dukan damuwoyinku da nawayarku da kuma faɗace-faɗacenku duka ni kaɗai? 13 Ku
zaɓi waɗansu masu hikima, masu ganewa, da kuma mutanen da ake girmama daga
kowace kabilarku, zan kuma sa su a kanku."

14 Kuka amsa mini, kuka ce, "Abin da ka ce za ka yi, yana da kyau."

15 Saboda haka na ɗauko shugabannin kabilanku masu hikima, waɗanda suka
saba da ma'amala da jama'a, na sa su shugabanni a gabanku, waɗansu suka zama
shugabanni a kan dubu-dubu, waɗansu a kan ɗari-ɗari, waɗansu a kan hamsin-
hamsin, waɗansu kuma a kan goma-goma. Na sa su zama shugabanni a kabilanku.
16 Na kuma umarci alƙalanku a wancan lokaci, na ce, "Ku yi adalci cikin shari'a
tsakanin 'yan'uwanku, ko damuwar tana tsakanin 'yan'uwa Isra'ilawa ne, ko kuwa
tsakanin Isra'ilawa da baƙin da suke zaune a cikinku. 17 Kada ku nuna sonkai a cikin
hukuncinku, ku saurari kowane ɓangare, babba da ƙarami, kada ku ji tsoron wani,
gama hukunci na Allah ne. Ku kawo kowane batun da ya sha ƙarfinku, zan kuwa
saurare shi." 18 A wancan lokacin kuwa na faɗa muku dukan abin da ya kamata ku
yi.

*An aiki 'yan leƙen asiri*
*(Kidaya 13.1-33)*

19 Sa'an nan, muka kama hanya daga Horeb muka ratsa wajen ƙasar tudun
Amoriyawa ta dukan hamadarta mai fāɗi, da kuma mai bantsoron da kuka gani,
muka kuma kai Kadesh Barneya yadda UBANGIJI, Allahnmu ya umarce mu. 20 Sai na
ce muku, "Kun iso ƙasar tudun Amoriyawa, wadda UBANGIJI, Allahnmu yake ba mu.

21 Duba, Ubangiji Allahnku ya ba ku ƙasar. Ku haura ku mallake ta yadda Ubangiji
Allahn kakanninku ya faɗa muku. Kada ku ji tsoro, kada ku fid da zuciya."
22 Sai dukanku kuka zo wurina kuka ce, "Bari mu aiki mutane su yi gaba su leƙi
mana asirin ƙasar, su kuma kawo mana labari game da hanyar da za mu bi, da kuma
biranen da za mu shiga."
23 Ra'ayin nan naku ya yi mini kyau, saboda haka na zaɓe ku goma sha biyu,
mutum guda daga kowace kabila. 24 Suka tafi, suka haura zuwa ƙasar tudu, suka
kai Kwarin Eshkol, suka leƙo asirin ƙasar. 25 Suka ɗebi 'ya'yan itatuwan ƙasar, suka
sauko mana da su, suka kuma ba da labari cewa, "Kasar da Ubangiji Allahnmu yake
ba mu, kyakkyawa ce."

*(Kidaya 14.1-45)*

26 Amma ba ku yi niyya ku haura ba, kuka yi tawaye gāba da umarnin Ubangiji
Allahnku. 27 Kuka yi gunaguni a cikin tentunanku, kuna cewa, "Ubangiji ya ƙi mu;
shi ya sa ya fitar da mu daga Masar don yǎ ba da mu ga hannuwan Amoriyawa
su hallaka mu. 28 Ina za mu? 'Yan'uwanmu suka sa muka fid da zuciya. Suka ce,
'Mutanen sun fi mu ƙarfi, sun kuma fi mu tsayi; biranen manya ne, da katanga har
sama. Mun ma ga Anakawa a can.' "
29 Sai na ce muku, "Kada ku firgita; kada ku ji tsoronsu. 30 Ubangiji Allahnku yana
a gabanku, zai yi yaƙi saboda ku, kamar yadda ya yi a kan idanunku a Masar, 31 da
kuma a cikin hamada. A can ma kun ga yadda Ubangiji Allahnku ya riƙe ku ko'ina
da kuka tafi, kamar yadda mahaifi yakan riƙe ɗansa, sai da kuka kai wannan wuri."
32 Duk da haka, ba ku amince da Ubangiji Allahnku ba, 33 shi da ya sha gabanku
a tafiyarku, cikin wuta da dad dare da kuma girgije da rana, don yǎ nemi wurare
domin ku kafa sansani, don kuma yǎ nuna muku hanyar da za ku bi.
34 Da Ubangiji ya ji abin da kuka faɗa, sai ya husata, ya kuma yi rantsuwa ya ce,
35 "Babu wani a cikin wannan muguwar tsara da zai ga ƙasa mai kyau da na rantse
zan ba wa kakanninku, 36 sai dai Kaleb ɗan Yefunne. Zai gan ta, zan ba shi duk ƙasar
da tafin ƙafarsa ta taka, shi da zuriyarsa, gama ya bi Ubangiji da zuciya ɗaya."
37 Saboda ku Ubangiji ya husata da ni, ya kuma ce, "Kai ma, ba za ka shiga ƙasar
ba. 38 Amma mataimakinka, Yoshuwa ɗan Nun, zai shiga. Ka ƙarfafa shi gama shi
ne zai jagoranci Isra'ila su gāje ta. 39 Amma 'ya'yanku ƙanana waɗanda ba su san
mugunta ko nagarta ba, waɗanda kuke tsammani za a kwashe su ganima, su za su
shiga ƙasar. Zan ba da ita gare su, za su kuwa mallake ta. 40 Amma ku kam, sai ku
juya, ku koma cikin hamada ta hanyar Jan Teku."
41 Sai kuka amsa, kuka ce, "Mun yi zunubi ga Ubangiji. Za mu haura mu yi yaƙi
yadda Ubangiji Allahnmu ya umarce mu." Saboda haka kowannenku ya yi ɗamara
da kayan yaƙinsa, kuka yi tsammani zai zama muku da sauƙi ku ci ƙasar tuddai da
yaƙi.
42 Amma Ubangiji ya ce mini, "In faɗa muku, 'Kada ku fāɗa musu da yaƙi, gama
ba zai kasance tare da ku ba. Idan kuka kuskura, abokan gābanku za su murƙushe
ku.' "
43 Sai na faɗa muku, amma ba ku saurara ba. Kuka yi tawaye ga umarnin Ubangiji,
a cikin jahilcinku kuwa kuka taka, kuka haura cikin ƙasar tudu. 44 Amoriyawan da
suke zama a waɗannan tuddai, suka fito kamar tarin ƙudan zuma gāba da ku, suka
kore ku, suka fatattake ku daga Seyir har zuwa Horma. 45 Kuka dawo, kuka yi kuka
a gaban Ubangiji, amma bai kula da ku ba, balle yǎ saurare ku. 46 Haka kuwa kuka
zauna a Kadesh kwanaki masu yawa, kuka ci lokaci a can.

# 2

*Yawo a cikin hamada*

1 Sai muka juya muka kama hanya, muka nufi hamada, ta hanyar Jan Teku* yadda
Ubangiji ya umarce ni. Da daɗewa muka yi ta yawo kewaye da ƙasar tudun Seyir.
2 Sai Ubangiji ya ce mini, 3 "Kun yi ta yawo kewaye da ƙasar tudun nan da daɗewa;
yanzu ku juya, ku nufi arewa. 4 Ka ba wa mutane waɗannan umarnai, ka ce, 'Kuna
gab da wucewa cikin yankin 'yan'uwanku, zuriyar Isuwa, wanda yake zama a Seyir.
Za su ji tsoronku, amma ku yi hankali 5 kada ku tsokane su da yaƙi, gama ba zan ba
ku wata ƙasa daga cikinsu ba, ba ma wadda za tă iya isa ku sa ƙafarku a kai. Na ba
wa Isuwa ƙasar tudu ta Seyir, ta zama tasa. 6 Duk abincin za ku ci, da ruwan da za
ku sha, za ku biya su.' "
7 Ubangiji Allahnku ya albarkace ku cikin dukan aikin hannuwanku. Ya kiyaye ku
cikin tafiyarku a duk fāɗin hamada. Waɗannan shekaru arba'in Ubangiji Allahnku
ya kasance tare da ku, ba kuwa kun rasa wani abu ba.
8 Saboda haka muka ci gaba, muka wuce 'yan'uwanmu, zuriyar Isuwa, wanda yake
zama a Seyir. Muka bar hanyar Araba, wadda ta haura daga Elat da Eziyon Geber,
muka nufi wajen hamadar Mowab.
9 Sai Ubangiji ya ce mini, "Kada ku dami Mowabawa, ko ku tsokane su da yaƙi,
gama ba zan ba ku wani sashe na ƙasarsu ba. Na ba da Ar ga zuriyar Lot, ta zama
mallakarsu."
10 (Emawa, mutane ne masu ƙarfi da kuma yawa, suna kuma da tsayi kamar
Anakawa, dā sun zauna a can. 11 Kamar Anakawa, su ma an ɗauka su Refahiyawa
ne, amma Mowab suna kiransu Emawa. 12 Haka ma Horiyawa, a dā sun zauna a
Seyir, amma zuriya Isuwa suka kore su. Suka hallaka Horiyawa da suke kafinsu,
suka kuma zauna a wurinsu, kamar dai yadda Isra'ila ta yi a ƙasar da Ubangiji ya
ba su a matsayin mallaka.)
13 Ubangiji kuwa ya ce, "Yanzu ku tashi ku ƙetare Kwarin Zered." Sai muka ƙetare
kwarin.
14 Dukan shekarun da muka yi a tafiyarmu daga Kadesh Barneya zuwa lokacin da
muka ƙetare Kwarin Zered, sun kai shekaru talatin da takwas. A lokacin, wannan
tsara gaba ɗaya ta mutanen da suka isa yaƙi sun mutu daga sansani, yadda Ubangiji
ya rantse musu. 15 Hannun Ubangiji ya yi gāba da su sai da ya hallaka su ƙaƙaf daga
sansani.
16 To, sa'ad da na ƙarshe cikin waɗannan mayaƙa a cikin mutanen ya rasu, 17 sai
Ubangiji ya ce mini, 18 "Yau za ku wuce ta yankin Mowab a Ar. 19 Sa'ad da kuka iso
kusa da Ammonawa, kada ku dame su, ko ku tsokane su da yaƙi, gama ba zan ba
ku mallakar wata ƙasar da take ta Ammonawa ba. Na riga na ba da ita mallaka ga
zuriyar Lot."
20 (Wannan ita ma a ɗauka ta a matsayin ƙasar Refahiyawa waɗanda dā sun zauna
a can ne; amma Ammonawa suna ce da su Zamzummawa. 21 Mutane ne masu ƙarfi
da kuma yawa, suna kuma da tsayi kamar Anakawa. Ubangiji ya hallaka su daga
gaban Ammonawa, waɗanda suka kore su, suka kuma zauna a wurinsu. 22 Ubangiji
ya yi daidai yadda ya yi wa zuriyar Isuwa waɗanda suka zauna a ƙasar Seyir, sa'ad
da ya hallaka Horiyawa a gabansu. Su kuma suka kore su, suka zauna a wurinsu.
Har wa yau, zuriyar Isuwa ne suke zama a can. 23 Kusan abu ɗaya ya faru, sa'ad
da Kaftorawa daga ƙasar Kaftor suka hallaka Awwiyawa, waɗanda dā suke zaune a
yankin ƙauyukan da suke kewaye da Gaza. Suka zauna a wurinsu.)

*Cin Sihon sarkin Heshbon da yaƙi*

24 "Ku fito yanzu ku ƙetare Kwarin Arnon. Duba, na ba da Sihon mutumin
Amoriyawa a hannunku, na kuma ba da sarkin Heshbon da ƙasarsa. Ku fara mallake
ta, ku kuma yi yaƙi da shi. 25 A wannan rana zan fara sa tsoro da fargabanku a kan

* **2:1** Da Ibraniyanci Yam Suf; wato, Tekun Iwa.

dukan al’ummai, a ƙarƙashin sama. Za su ji labarinku, za su yi rawan jiki, su kuma
damu saboda ku.”

*(Kidaya 21.21-30)*

26 Daga hamadar Kedemot, na aiki ’yan saƙo zuwa wurin Sihon sarkin Heshbon,
a kan ina neman zaman lafiya, ina cewa, 27 “Bari mu wuce cikin ƙasarka. Za mu
bi ta kan hanya ne kaɗai; ba za mu ratse dama ko hagu ba. 28 Ka sayar mana da
abincin da za mu ci, da kuma ruwan da za mu sha a farashinsu na azurfa. Ka dai bar
mu mu wuce ta ƙasarka kawai, 29 kamar yadda zuriyar Isuwa, waɗanda suke zaune
a Seyir, da Mowabawa, waɗanda suke zaune a Ar, suka yardar mana, gama muna
so mu ƙetare Urdun zuwa ƙasa wadda UBANGIJI, Allahnmu yake ba mu.” 30 Amma
Sihon sarkin Heshbon ya ƙi yă bar mu mu wuce a ciki. Gama UBANGIJI Allahnku ya
sa ruhunsa ya taurare don yă ba da shi a hannuwanku kamar yadda ya yi yanzu.

31 UBANGIJI ya ce mini, “Duba, na fara ba da Sihon da ƙasarsa gare ku. Yanzu ku
fara cinta, ku kuma mallake ƙasarsa.”

32 Sa’ad da Sihon da dukan sojojinsa suka fito don su sadu da mu, a yaƙi, a Yahaz,
33 sai UBANGIJI Allahnmu ya ba da shi gare mu, muka kuwa buga shi tare da ’ya’yansa
maza da kuma dukan sojojinsa. 34 A wannan lokaci mun ci dukan biranensa, muka
kuma hallaka su, maza, mata da kuma yara. Ba mu bar wani da rai ba. 35 Amma
muka washe, muka kuma kwasa shanu da kuma ganima daga biranen wa kanmu.
36 UBANGIJI Allahnmu ya taimake mu muka ci Arower wadda take a gefen Kwarin
Arnon, da garin da yake a cikin kwarin, har zuwa Gileyad. Babu garin da ya gaggare
mu. 37 Amma bisa ga umarnin UBANGIJI Allahnmu, ba ku yi kusa da wata ƙasar
Ammonawa, ko ƙasar da take gefen kwarin kogin Yabbok, ko kuwa wadda take
kewaye da birane cikin tuddai ba.

# 3

*Cin Og sarkin Bashan da yaƙi*
*(Kidaya 21.31-35)*

1 Biye da wannan muka juya muka haura ta hanyar wajen Bashan, inda Og, sarkin
Bashan tare da dukan mayaƙansa suka fito don su sadu da mu a yaƙi, a Edireyi.
2 UBANGIJI ya ce mini, “Kada ka ji tsoronsa, gama na riga na miƙa shi da dukan
mayaƙansa da kuma ƙasarsa gare ka. Yi masa abin da ka yi wa Sihon sarkin
Amoriyawa, wanda ya yi mulkin Heshbon.”

3 Saboda haka UBANGIJI Allahnmu ya ba da Og, sarkin Bashan da dukan mayaƙansa
a hannuwanmu. Muka karkashe su, ba mu bar wani da rai ba. 4 A wannan lokaci
muka kwashe dukan biranensa. Babu ɗaya daga birane sittin da ba mu ɗauke daga
gare su ba, dukan yankin Argob, masarautar Og a Bashan. 5 Dukan biranen nan masu
katanga da suke da tsayi masu ƙofofi da ƙyamare, akwai kuma manya ƙauyukan da
ba su da katanga. 6 Muka hallaka su ƙaƙaf, kamar yadda muka yi wa Sihon sarkin
Heshbon, muka hallaka kowace birni, maza, mata da yara. 7 Amma dukan dabbobin
da kuma ganimar daga biranensu muka kwaso wa kanmu.

8 A lokacin ne muka ƙwace wannan ƙasa daga hannun sarakunan nan biyu na
Amoriyawa, wato, ƙasa wadda take a hayin Urdun, daga Kwarin Arnon zuwa Dutsen
Hermon. 9 (Hermon ne Sidoniyawa suke kira Siriyon, Amoriyawa kuwa suna kira shi
Senir.) 10 Muka kama dukan biranen da suke kan tudu, da dukan Gileyad, da dukan
Bashan, har zuwa Saleka da Edireyi, biranen masarautar Og a Bashan. 11 (Og sarkin
Bashan, ne kaɗai ya ragu cikin Refahiyawa. An yi gadonsa da ƙarfe, tsawon gadon ya
fi ƙafa goma sha uku, fāɗinsa kuwa ƙafa shida ne. Yana nan a Rabba ta Ammonawa
har yanzu.)

### *Rabawa ƙasar*
### *(Kidaya 32.1-42)*

12 Cikin ƙasar da muka kwasa a lokacin, na ba wa mutanen Ruben da mutanen
Gad yankin arewa na Arower ta Kwarin Arnon, haɗe da rabin ƙasar tudu ta Gileyad,
tare da biranenta. 13 Sai kuma na ba wa rabin kabilar Manasse sauran rabin ƙasar
tudu ta Gileyad da kuma dukan Bashan, masarautar Og (Wato, dukan yankin ƙasan
nan na Argob a Bashan da dā ake kira ƙasar Refahiyawa. 14 Yayir na zuriyar
Manasse ya karɓi dukan yankin ƙasar Argob a Bashan har zuwa iyakar Geshurawa
da Ma’akatiyawa. Sai ya kira ƙauyukan wurin da sunansa, Hawwot Yayir.)* 15 Na
kuma ba da Gileyad ga Makir. 16 Amma ga mutanen Ruben da mutanen Gad, na ba
da yankin da ya tashi daga Gileyad, ya gangara zuwa Kwarin Arnon (tsakiyar kwarin
kuwa shi ne iyaka) ya fita zuwa Kogin Yabbok, wanda yake shi ne iyakar Ammonawa.
17 Iyakarsa daga yamma kuwa shi ne Urdun a Araba, daga Kinneret zuwa Tekun
Araba (wato, Tekun Gishiri) a gangaren gindin Dutsen Fisga wajen gabas.

18 Na umarce ku a lokacin na ce, “Ubangiji Allahnku ya ba ku wannan ƙasa ku
mallake ta. Dukan mayaƙanku za su haye da shirin yaƙi a gaban ’yan’uwanku,
Isra’ilawa. 19 Amma matanku, yaranku da dabbobinku (na sani kuna da dabbobi
masu yawa), su ne za ku bari a garuruwan da na ba ku, 20 sai Ubangiji ya ba da
hutu ga sauran ’yan’uwanku, yadda ya yi da ku, su ma suka sami ƙasar da Ubangiji
Allahnku yake ba su, a ƙetaren Urdun, sa’an nan kowannenku zai komo ga mallakar
da na ba ku.”

### *An hana Musa ƙetare Urdun*

21 A lokacin nan na umarci Yoshuwa na ce, “Da idanunka ka ga dukan abin da
Ubangiji Allahnku ya yi da waɗannan sarakuna biyu. Haka Ubangiji zai yi da dukan
masarautai a can, inda za ku. 22 Kada ku ji tsoronsu, gama Ubangiji Allahnku zai yi
yaƙi dominku.”

23 A lokacin, na roƙi Ubangiji na ce, 24 “Ya Ubangiji Mai Iko Duka, ka fara nuna
wa bawanka ɗaukakarka da ikonka. Akwai wani allah a sama ko a duniya, wanda
zai aikata waɗannan manyan ayyukan kamar ka? 25 Ina roƙonka, bari in ƙetare in
ga ƙasa mai kyau ɗin nan a ƙetaren Urdun, wannan ƙasar mai kyau ta tuddai, da
kuma Lebanon.”

26 Amma saboda ku, Ubangiji ya yi fushi da ni, bai kuwa saurare ni ba. Sai Ubangiji
ya ce, “Ya isa haka, kada ka ƙara yin magana da ni game da wannan batu. 27 Haura
zuwa ƙwanƙolin Fisga, ka dubi ƙasar da idanunka daga kowane gefe, yamma, da
arewa, da kudu, da kuma gabas, gama ba za ka ƙetare wannan Urdun ba. 28 Amma
ka umarci Yoshuwa, ka ƙarfafa shi, ka kuma ba shi ƙarfin gwiwa, gama shi ne zai
jagoranci wannan mutane su haye, yă kuma ba su gādon ƙasar da za ka gani.” 29 Sai
muka zauna a kwari kusa da Bet-Feyor.

# 4

### *An umarta a yi biyayya*

1 To, ku ji, ya Isra’ila, ku kasa kunne ga ƙa’idodi da dokokin da nake shirin koya
muku. Ku bi su domin ku yi tsawon rai, ku kuma shiga ku mallaki ƙasar da Ubangiji,
Allahn kakanninku yake ba ku. 2 Kada ku ƙara, kada ku rage daga cikin abin da nake
umarce ku. Amma ku kiyaye umarnan nan na Ubangiji Allahnku, da na ba ku.

3 Da idanunku, kun ga abin da Ubangiji ya yi a Ba’al-Feyor. Yadda Ubangiji Allahnku
ya hallaka waɗansu daga cikinku waɗanda suka yi wa Ba’al-Feyor sujada, 4 Amma
ku da kuka manne ga Ubangiji Allahnku, kuna da rai har wa yau.

* **3:14** Ko kuwa kira mazaunin Yayir

5 Ga shi, na koya muku ƙa'idodi da dokoki, yadda Ubangiji Allahna ya umarce ni,
don ku bi su a ƙasar da za ku shiga ku mallaki. 6 Ku kiyaye su, ku aikata su, gama
yin haka zai tabbatar wa sauran al'ummai, kuna da hikima da ganewa. Sa'ad da
al'ummai za su ji waɗannan dokoki, za su ce, "Ba shakka, wannan babbar al'umma
tana da hikima da ganewa." 7 Wace al'umma ce mai girma haka wadda allolinta take
kusa da su yadda Ubangiji Allahnmu yake kusa da mu a duk sa'ad da muka yi addu'a
gare shi? 8 Wace al'umma ce mai girma haka wadda take da ƙa'idodi da dokoki masu
adalci kamar waɗannan ƙunshin dokokin da nake sa a gabanku a yau?
9 Ku kula, ku kuma lura da kanku sosai, don kada ku manta da abubuwan da
idanunku suka gani, ko kuwa ku bari su fita daga zuciyarku muddin ranku. Ku
koyar da su ga 'ya'yanku, da 'ya'yan 'ya'yanku. 10 Ku tuna da ranar da kuka tsaya
a gaban Ubangiji Allahnku a Horeb, sa'ad da ya ce mini, "Ka tara mutane a gabana,
don su ji maganata, su koya yin mini bangirma muddin ransu a ƙasar, su kuma iya
koyar da su ga 'ya'yansu." 11 Sai kuka matso kusa, kuka tsaya a gindin dutse yayinda
yana cin wuta har zuwa sararin sama, ga kuma baƙin gizagizai da kuma baƙin duhu.
12 Sai Ubangiji ya yi magana daga wutar. Kuka ji furcin kalmomin, amma ba ku ga
siffar kome ba, sai dai murya kaɗai kuka ji. 13 Ya furta alkawarinsa gare ku, Dokoki
Goma, waɗanda ya umarce ku ku bi, ya kuma rubuta su a alluna biyu. 14 Sa'an nan
Ubangiji ya umarce ni a wannan lokaci, in koya muku ƙa'idodi da dokokin da za ku
bi a ƙasar da kuke hayewa Urdun don mallake.

### *An hana bautar gumaka*

15 Ba ku ga wata siffa a ranar da Ubangiji ya yi magana da ku a Horeb daga wuta
ba. Saboda haka ku lura da kanku sosai, 16 don kada ku lalace, ku kuma yi wa
kanku gunki, siffa ta wani kama, ko a kamannin namiji, ko kuwa ta mace, 17 ko
a kamannin wata dabba a duniya, ko na wani tsuntsun da yake tashi a sama, 18 ko
kuwa a kamannin wata halittar da take rarrafe a ƙasa, ko na wani kifi a cikin ruwaye
a ƙarƙashi. 19 Sa'ad da kuka ɗaga ido kuka kali sama, kuka ga rana da wata, da
taurari, da dukan halittun sama, sai ku kula fa, kada ku jarrabtu, ku ce za ku yi musu
sujada, ko ku bauta musu; abubuwan nan Ubangiji Allahnku ne ya rarraba wa dukan
al'umman da suke ko'ina a ƙarƙashin sararin sama. 20 Amma ku, Ubangiji ya ɗauke
ku, ya fid da ku daga matuya mai narken ƙarfe, wato, daga Masar, domin ku zama
jama'arsa ta musamman kamar yadda kuke a yau.
21 Ubangiji ya yi fushi da ni saboda ku, ya kuma yi rantsuwa cewa ba zan haye
Urdun, in shiga ƙasan nan mai kyau da Ubangiji Allahnku yake ba ku gādo ba. 22 Zan
mutu a wannan ƙasa; ba zan haye Urdun ba; amma kuna gab da ƙetarewa, ku
mallaki wannan ƙasa mai kyau. 23 Ku yi hankali kada ku manta da alkawarin da
Ubangiji Allahnku ya yi da ku; kada fa ku yi wa kanku gunki a kamannin wani abin
da Ubangiji Allahnku ya hana. 24 Gama Ubangiji Allahnku wuta ne mai ƙuna, Allah
ne mai kishi.
25 Bayan kun haifi 'ya'ya da jikoki, kuka kuma zauna na dogon lokaci a ƙasar, in
har kuka lalace, kuka kuma yi wani irin gunki, kuna aikata mugunta a gaban Ubangiji
Allahnku, kuna kuma sa shi fushi. 26 Yau, na kira sama da duniya, su zama shaidata
a kanku. Idan kuka yi rashin biyayya, lalle za ku hallaka nan da nan daga ƙasar da
kuke ƙetare Urdun ku gāda. Ba za ku daɗe a cikinta ba, amma za a kawar da ku
ƙaƙaf. 27 Ubangiji zai watsar da ku a cikin mutane, ɗan kaɗan ne kaɗai za su ragu a
cikin al'umman da Ubangiji zai kai ku. 28 A can za ku bauta wa allolin da mutum ya
yi, na itace da dutse da ba sa gani, ba sa ji, ba sa ci, ba kuma iya sansanawa. 29 Amma
daga can in kuka nemi Ubangiji Allahnku, da dukan zuciyarku da kuma dukan ranku,
za ku same shi. 30 Sa'ad da kuke cikin wahala saboda waɗannan abubuwan da suka
same ku nan gaba, to, sai ku juyo ga Ubangiji Allahnku, ku kuma yi masa biyayya.

31 Gama UBANGIJI Allahnku, Allah ne mai jinƙai; ba zai yashe ku ko yă hallaka, ko
kuma yă manta da alkawarin da ya yi da kakanninku, wanda ya tabbatar da su da
rantsuwa ba.

*UBANGIJI Allah ne*

32 Ku bincika dukan tarihi mana, tun daga lokacin da Allah ya halicci mutane a
cikin duniya har yă zuwa yanzu; ku tantambaya daga wannan kusurwa ta samaniya
zuwa waccan, ko wani babban abu irin wannan ya taɓa faruwa, ko kuma an taɓa
jin labarin irinsa? 33 Akwai waɗansu mutanen da suka taɓa jin muryar Allah yana
magana daga wuta, kamar yadda kuka ji har suka rayu? 34 Akwai wani allahn da
ya taɓa yin ƙoƙari yă ɗauko wa kansa wata al'umma daga wata al'umma, ta wurin
gwaje-gwaje, ta wurin alamu masu banmamaki da al'ajabai, ta wurin yaƙi, ta wurin
hannu mai iko, da kuma hannu mai ƙarfi, ko kuwa ta wurin ayyuka masu bangirma
da na banmamaki, kamar dukan abubuwan da UBANGIJI Allahnku ya yi saboda ku a
Masar, a kan idanunku?
35 An nuna muku dukan waɗannan abubuwa saboda ku san cewa UBANGIJI, shi ne
Allah; ban da shi, babu wani. 36 Daga sama ya sa kuka ji muryarsa, don yă hore ku.
A duniya ya nuna muku wutarsa mai girma, kuka kuma ji kalmominsa daga wuta.
37 Domin ya ƙaunaci kakanninku, ya kuma zaɓi zuriyarsu a bayansu, ya fitar da ku
daga Masar ta wurin kasancewarsa da kuma ƙarfinsa mai girma, 38 don yă fitar da
ku a gaban al'ummai da suka fi ku girma da kuma ƙarfi, ya kawo ku cikin ƙasarsu,
don yă ba ku ita ta zama gādonku, kamar yadda yake a yau.
39 Ku sani, ku kuma riƙe a zuciya a wannan rana, cewa UBANGIJI shi ne Allah a
sama da kuma a ƙasa. Babu wani kuma. 40 Ku kiyaye ƙa'idodi da umarnai, waɗanda
nake ba ku a yau, domin zaman lafiyarku da kuma na zuriyarku bayan ba ku, domin
kuma ku yi tsawon rai a ƙasa wadda UBANGIJI Allahnku yake ba ku har abada.

*Biranen mafaka*

41 Sa'an nan Musa ya keɓe birane uku gabas da Urdun, 42 waɗanda duk wanda
ya yi kisankai, in ba da gangan ba ne ya kashe maƙwabcinsa, wanda babu ƙiyayya
tsakaninsu a dā, zai iya gudu zuwa. Zai iya gudu zuwa cikin ɗaya daga waɗannan
birane, yă tsira da ransa. 43 Biranen kuwa su ne, Bezer a dutsen hamada, don
mutanen Ruben; Ramot Gileyad, don mutanen Gad; da kuma Golan a Bashan, don
mutanen Manasse.

*Gabatarwa ga doka*

44 Wannan ita ce dokar da Musa ya sa a gaban Isra'ilawa. 45 Waɗannan su ne
farillai, ƙa'idodi da kuma dokokin da Musa ya ba su, sa'ad da suka fito daga Masar.
46 Sa'ad da suke a kwari kusa da Bet-Feyor, gabas da Urdun, a ƙasar Sihon sarkin
Amoriyawa, wanda ya yi mulki a Heshbon, da Musa da Isra'ilawa suka ci da yaƙi
sa'ad da suka fito daga Masar. 47 Suka mallaki ƙasarsa da kuma ƙasar Og sarkin
Bashan, sarakuna biyu na Amoriyawa, gabas da Urdun. 48 Wannan ƙasa ta tashi daga
Arower a kewayen Kwarin Arnon zuwa Dutsen Siyon* (wato, Hermon), 49 ya kuma
haɗa da dukan Araba† gabas da Urdun, har zuwa tekun Araba a gindin gangaren
Fisga.

# 5

*Dokoki goma*
*(Fitowa 20.1-17)*

1 Musa ya tattara dukan Isra'ila ya ce,

---

* **4:48** Da Ibraniyanci; Siriyak (dubi kuma M Sh 3.9) Siriyon † **4:49** Wato, Bahar Maliya

Ku ji, ya Isra'ila, ƙa'idodi da dokokin da na furta a kunnuwanku a yau. Ku koye su,
ku kuma tabbata kun bi su. 2 UBANGIJI Allahnmu ya yi alkawari da mu a Horeb. 3 Ba
da kakanninmu ba ne UBANGIJI ya yi wannan alkawari, amma da mu ne, da dukanmu
waɗanda muke da rai a yau. 4 UBANGIJI ya yi magana fuska da fuska da ku daga wuta
a kan dutse. 5 (A wannan lokaci na tsaya tsakanin UBANGIJI da ku, don in furta muku
maganar UBANGIJI, domin kun ji tsoron wutar, ba ku kuwa hau dutsen ba.)
Ya ce,

6 "Ni ne UBANGIJI Allahnka, wanda ya fitar da ku daga Masar, daga ƙasar bauta.

7 "Ba za ka kasance da waɗansu alloli a gabana* ba.
8 Ba za ka yi wa kanka gunki, ko wata siffar abin da take a sama a bisa, ko siffar abin da yake a duniya a ƙasa, ko siffar abin da yake a cikin ruwa a ƙarƙashin
ƙasa ba. 9 Ba za ka rusuna musu, ko ka yi musu sujada ba. Gama Ni, UBANGIJI Allahnka, Allah ne mai kishi, nakan hukunta 'ya'ya saboda zunuban iyaye har
tsara ta uku da ta huɗu na waɗanda suka ƙi ni. 10 Amma nakan nuna ƙauna ga dubban tsararraki na waɗanda suke ƙaunata, suke kuma kiyaye dokokina.
11 Ba za ka yi amfani da sunan UBANGIJI Allahnka a banza ba, gama UBANGIJI zai ba wa duk mai yin amfani da sunansa a banza laifi.
12 Ka kiyaye ranar Asabbaci ta wurin kiyaye ta da tsarki, yadda UBANGIJI Allahnka
ya umarce ka. 13 Kwanaki shida za ka yi aiki, ka kuma yi dukan aikinka, 14 amma rana ta bakwai, Asabbaci ne ga UBANGIJI Allahnka. A kanta ba za ka yi wani aiki ba, ko kai, ko ɗanka, ko 'yarka, ko bawanka, ko baiwarka, ko saniyarka, ko jakinka, ko wani daga dabbobinka, ko baƙo a ƙofofinka, don bayinka maza da
mata su ma su huta, kamar ka. 15 Ka tuna fa, dā kai bawa ne a ƙasar Masar amma UBANGIJI Allahnka ya fitar da kai daga can da iko da kuma ƙarfi. Saboda haka UBANGIJI Allahnka ya umarce ka ka kiyaye ranar Asabbaci.
16 Ka ba da girma ga mahaifinka da mahaifiyarka, yadda UBANGIJI Allahnka ya umarce ka, don ka yi tsawon rai, ka kuma sami zaman lafiya a ƙasar da UBANGIJI Allahnka yake ba ka.
17 Kada ka yi kisankai.
18 Kada ka yi zina.
19 Kada ka yi sata.
20 Kada ka ba da shaidar ƙarya a kan maƙwabcinka.
21 Kada ka yi ƙyashin matar maƙwabcinka. Kada kuma ka yi sha'awar gidan maƙwabcinka, ko gonarsa, ko bayinsa maza da mata, ko saniyarka, ko jakinsa, ko dai wani abin da yake na maƙwabtanka."

22 Waɗannan su ne dokokin da UBANGIJI ya furta da babbar murya ga taronku gaba
ɗaya, a can dutse ta tsakiyar wuta, girgije da kuma baƙin duhu; bai kuma ƙara kome
ba. Sa'an nan ya rubuta su a kan alluna biyu na dutse, ya kuma ba ni su.
*(Fitowa 20.18-21)*
23 Sa'ad da kuka ji muryar daga duhu, yayinda dutsen yana cin wuta, dukan
manyan kabilanku da dattawanku suka zo wurina. 24 Kuka kuma ce, "UBANGIJI
Allahnmu ya nuna mana ɗaukakarsa da zatinsa, mun kuma ji muryarsa a tsakiyar
wutar. A yau mun ga cewa mutum zai iya rayu idan ma Allah ya yi magana da shi.
25 Amma yanzu, don me za mu mutu? Wannan wuta mai girma za tă cinye mu, za
mu kuwa mutu in muka ci gaba da jin muryar UBANGIJI Allahnmu. 26 Gama wanda

* **5:7** Ko kuwa in ban da ni

ɗan adam ne ya taɓa jin muryar Allah mai rai yana magana daga wuta, kamar yadda
muka ji, ya kuma tsira? 27 Kai, ka matsa kusa, ka saurara ga dukan abin da UBANGIJI
Allahnmu ya faɗa. Sa'an nan ka faɗa mana dukan abin da UBANGIJI Allahnmu ya
faɗa maka. Za mu saurara, mu kuma yi biyayya."
28 UBANGIJI ya ji ku, sa'ad da kuka yi magana da ni, sai UBANGIJI ya ce mini, "Na ji
abin da wannan mutane suka faɗa maka. Abin da suka faɗa daidai ne. 29 Kash, da
a ce zukatansu za su zama masu tsorona, su kuma kiyaye dukan dokokina kullum
mana, saboda kome yǎ zama da lafiya gare su, da kuma 'ya'yansu har abada!
30 "Je, ka faɗa musu su koma tentunansu. 31 Kai kuwa ka tsaya a nan tare da ni
saboda in ba ka umarnai, ƙa'idodi da kuma dokoki duka, da za ka koya musu don su
bi a ƙasar da nake ba su, su mallaka."
32 Sai ku yi hankali don ku yi abin da UBANGIJI Allahnku ya umarce ku; kada ku juya
dama ko hagu. 33 Ku yi tafiya cikin dukan hanyar da UBANGIJI Allahnku ya umarce
ku, saboda ku zauna, ku yi nasara, ku kuma yi tsawon rai a ƙasar da za ku mallaka.

# 6

*Kaunaci UBANGIJI Allahnka*
1 Waɗannan su ne umarnai, ƙa'idodi da kuma dokokin da UBANGIJI Allahnku ya
umarce ni in koya muku don ku kiyaye a ƙasar da kuke haye Urdun don mallaka,
2 saboda ku, 'ya'yanku, da kuma 'ya'yansu bayansu za su ji tsoron UBANGIJI Allahnku
muddin kuna rayuwa ta wurin kiyaye dukan ƙa'idodinsa da umarnan da na ba ku,
da kuma don ku yi tsawon rai. 3 Ku ji, ya Isra'ila, ku kuma kula, ku kiyaye su don
yǎ zama muku da lafiya, ku kuma ƙaru sosai a ƙasa mai zub da madara da zuma,
kamar dai yadda UBANGIJI, Allahn kakanninku ya yi muku alkawari.
4 Ku ji, ya Isra'ila, UBANGIJI Allahnmu, UBANGIJI ɗaya ne. 5 Ku ƙaunaci
UBANGIJI Allahnku da dukan zuciyarku, da dukan ranku, da kuma dukan ƙarfinku.
6 Waɗannan umarnai da nake ba ku a yau, za su kasance a zukatanku. 7 Ku koya wa
'ya'yanku su da himma. Yi musu magana game da su sa'ad da kuke zaune a gida,
da sa'ad da kuke tafiya a hanya, sa'ad da kuke kwance, da sa'ad da kuka tashi. 8 Ku
ɗaura su su zama alamu a hannuwanku, ku kuma ɗaura su a goshinku. 9 Ku rubuta
su a dogaran ƙofofin gidajenku, da ƙofofinku.
10 Sa'ad da UBANGIJI Allahnku ya kawo ku cikin ƙasar da ya rantse ga kakanninku,
ga Ibrahim, Ishaku da Yaƙub, yǎ ba ku, ƙasa mai girma, mai manyan biranen da ba
ku kuka gina ba, 11 gidaje cike da kowane irin abubuwa masu kyau, da ba ku kuka
tanadar ba, rijiyoyin da ba ku kuka haƙa ba, da gonakin inabi da itatuwan zaitun da
ba ku kuka shuka ba, sa'ad da kuwa kuka ci, kuka kuma ƙoshi, 12 ku yi hankali cewa
ba ku manta da UBANGIJI wanda ya fitar da ku daga Masar, da gidan bauta ba.
13 Ku ji tsoron UBANGIJI Allahnku, ku bauta masa shi kaɗai, ku kuma yi alkawaranku
da sunansa. 14 Kada ku bi waɗansu alloli, allolin mutanen da suke kewaye da ku;
15 gama UBANGIJI Allahnku, wanda yake cikinku, Allah ne mai kishi, fushinsa kuma
zai yi ƙuna gāba da ku, zai kuma hallaka ku daga fuskar ƙasar. 16 Kada ku gwada
UBANGIJI Allahnku kamar yadda kuka yi a Massa. 17 Ku tabbata kun kiyaye umarnan
UBANGIJI Allahnku, da farillansa da kuma ƙa'idodinsa da ya ba ku. 18 Ku aikata abin
da yake daidai da kuma mai kyau a idon UBANGIJI, don yǎ zama muka da lafiya,
ku kuwa shiga ku mallaki ƙasa mai kyau da UBANGIJI ya yi alkawari da rantsuwa
ga kakanninku. 19 Zai kuwa korin dukan abokan gābanku da suke gabanku, yadda
UBANGIJI ya faɗa.
20 Nan gaba, sa'ad da 'ya'yanku suka tambaye ku, "Mene ne ma'anar farillai,
ƙa'idodi da kuma dokokin da UBANGIJI Allahnmu ya umarce ku?" 21 Sai ku gaya
musu, "Dā mu bayin Fir'auna ne a Masar, amma UBANGIJI ya fitar da mu daga

Masar da hannu masu ƙarfi. 22 A idanunmu UBANGIJI ya aikata manyan alamu
masu banmamaki, da al'ajabai gāba da Masarawa, da Fir'auna, da kuma dukan
gidansa. 23 Amma ya fitar da mu daga can domin yă kawo mu cikin ƙasar da ya yi wa
kakanninmu alkawari tare da rantsuwa zai ba mu. 24 UBANGIJI ya umarce mu mu yi
biyayya da dukan waɗannan ƙa'idodi, mu kuma ji tsoron UBANGIJI Allahnmu, saboda
kullum mu ci gaba, a kuma bar mu da rai, kamar yadda yake a yau. 25 In kuma muka
kula, muka kiyaye dukan dokokin nan a gaban UBANGIJI Allahnmu, kamar yadda ya
umarce mu, wannan zai zama adalci a gare mu."

# 7

*Korin al'ummai*
*(Fitowa 34.11-16)*

1 Sa'ad da UBANGIJI Allahnku ya kawo ku ƙasar da kuke shiga don ku mallaka,
ya kuma kori al'ummai masu yawa a gabanku; wato, Hittiyawa, Girgashiyawa,
Amoriyawa, Kan'aniyawa, Ferizziyawa, Hiwiyawa da Yebusiyawa, al'ummai bakwai
masu girma da ƙarfi fiye da ku. 2 Sa'ad da kuma UBANGIJI Allahnku ya ba da su
gare ku, kuka kuma ci su da yaƙi, sai ku hallaka su ƙaƙaf. Kada ku yi yarjejjeniya
da su, kada kuma ku nuna musu jinƙai. 3 Kada ku yi auratayya da su. Kada ku ba
da 'ya'yanku mata wa 'ya'yansu maza, ko ku ɗauko 'ya'yansu mata wa 'ya'yanku
maza. 4 Gama za su juye 'ya'yanku maza daga bina, su bauta waɗansu alloli, fushin
UBANGIJI kuma zai ƙuna a kanku da sauri, zai kuma hallaka ku. 5 Ga abin da za ku yi
da su, za ku rurrushe bagadansu, ku ragargaza keɓaɓɓun duwatsunsu, ku farfashe
ginshiƙan Asheransu, ku kuma ƙona gumakansu da wuta. 6 Gama ku mutane masu
tsarki ne ga UBANGIJI Allahnku. UBANGIJI Allahnku ya zaɓe ku daga dukan mutane a
fuskar duniya, don ku zama mutanensa, kayan gādonsa.

7 Ba don kun fi sauran al'ummai yawa ne ya sa UBANGIJI ya ƙaunace ku, ya kuma
zaɓe ku ba, gama ku ne mafi ƙanƙanta cikin dukan al'ummai. 8 Amma ya zama haka
domin UBANGIJI ya ƙaunace ku, ya kuma kiyaye rantsuwar da ya yi wa kakanninku
da ya fitar da ku da hannu mai ƙarfi, ya kuma cece ku daga ƙasar bauta, daga ikon
Fir'auna sarkin Masar. 9 Saboda haka, ku sani cewa UBANGIJI Allahnku, shi ne Allah;
shi Allah ne mai aminci, yana kiyaye alkawarinsa na ƙauna ga tsararraki dubu na
waɗanda suke ƙaunarsa suke kuma kiyaye umarnansa. 10 Amma
waɗanda suke ƙinsa, a fili yakan sāka musu da hallaka;
ba zai yi jinkiri yin ramuwa a kan maƙiyinsa ba, zai yi ramuwar a fili.
11 Saboda haka, sai ku lura, ku bi umarnai, ƙa'idodi, da dokokin nan da nake ba ku
a yau.

*(Maimaitawar Shari'a 28.1-14; Firistoci 26.3-13)*

12 In kuka mai da hankali ga waɗannan dokoki, kuka kuma yi hankali ga bin su, to,
UBANGIJI Allahnku zai kiyaye alkawarinsa na ƙauna gare ku, kamar yadda ya rantse
wa kakanninku. 13 Zai ƙaunace ku, yă albarkace ku, yă kuma ƙara yawanku. Zai
albarkaci 'ya'yanku, amfanin gonarku; hatsinku, sabon ruwan inabinku da kuma
mai, ƙanana shanunku, da 'yan tumaki na tumakinku, a ƙasar da ya rantse wa
kakanninku cewa zai ba ku. 14 Za a albarkace ku fiye da waɗansu mutane; babu
wani cikin maza ko matanku da zai kasance babu haihuwa, ba kuwa wata dabbarku
da za tă kasance babu haihuwa. 15 UBANGIJI zai kiyaye ku daga kowace cuta. Ba zai
wahalshe ku da mugayen cututtukan da kuka sani a Masar ba, amma zai aukar wa
dukan maƙiyanku. 16 Dole ku hallaka dukan mutanen da UBANGIJI Allahnku ya bashe
su gare ku. Kada ku ji tausayinsu, kada kuma ku bauta wa allolinsu, gama wannan
zai zama tarko gare ku.

[17] Wataƙila ku ce wa kanku, "Waɗannan al'ummai sun fi mu ƙarfi. Yaya za mu
kore su?" [18] Amma kada ku ji tsoronsu; ku tuna da kyau abin da UBANGIJI Allahnku
ya yi wa Fir'auna da kuma dukan Masar. [19] Kun ga da idanunku, manyan gwaje-
gwaje, alamu masu banmamaki da al'ajabai, hannu mai ƙarfi da kuma mai ikon da
UBANGIJI Allahnku ya fitar da ku. UBANGIJI Allahnku zai yi haka ga dukan mutanen
da yanzu kuke tsoro. [20] Ban da haka ma, UBANGIJI Allahnku zai aika da rina a cikinsu,
har sai sun hallaka sauran mutanen da suka ragu, waɗanda suka ɓuya daga gare ku.
[21] Kada ku tsorata saboda su, gama UBANGIJI Allahnku, wanda yake a cikinku, Allah
ne mai girma da kuma mai banrazana. [22] Da kaɗan da kaɗan UBANGIJI Allahnku zai
kore waɗannan al'ummai a gabanku. Ba a bari ku hallaka su duka gaba ɗaya ba,
in ba haka namun jeji za su yaɗu kewaye da ku. [23] Amma UBANGIJI Allahnku zai ba
da su gare ku, yana jefa su cikin rikicewa mai girma, har sai an hallaka su. [24] Zai
ba da sarakunsu a hannunku, za ku kuwa shafe sunayensu daga duniya. Babu wani
da zai yi tsayayya da ku, za ku hallaka su. [25] Ku ƙone siffar allolinsu da wuta. Kada
ku yi ƙyashin azurfa ko zinariyar da aka rufe allolin da ita, Kada ku kwashe su, don
kada su zamar muku tarko, gama abin ƙyama ne ga UBANGIJI Allahnku. [26] Kada ku
kawo abin ƙyama cikin gidajenku, domin kada ku zama kamar su. Gaba ɗaya ku yi
ƙyamarsu, ku ƙi su, gama an ware su, sun zama domin a hallaka.

# 8

*Kada ku manta da UBANGIJI*

[1] Ku hankali, ku bi kowane umarnin da nake ba ku a yau, saboda ku rayu, ku
ƙaru, ku kuma shiga, ku mallaki ƙasar da UBANGIJI ya alkawarta da rantsuwa ga
kakanninku. [2] Ku tuna yadda UBANGIJI Allahnku ya bishe ku a dukan hanya, a cikin
hamada waɗannan shekaru arba'in, don yă ƙasƙantar da ku, yă kuma gwada ku don
yă san abin da yake a zuciyarku, ko za ku kiyaye umarnansa, ko babu. [3] Ya ƙasƙantar
da ku, ya bar ku da yunwa, sa'an nan ya ciyar da ku da Manna, wadda ku, ko
kakanninku, ba su sani ba, ta haka ne ya sa kuka sani cewa, ba da abinci kaɗai mutum
zai rayu ba, amma ta wurin kowace kalmar da ta fito daga bakin UBANGIJI. [4] Tufafinku
ba su yayyage ba, ƙafafunku kuma ba su kumbura ba a waɗannan shekaru arba'in.
[5] Sai ku sani fa a cikin zuciyarku cewa kamar yadda mutum kan horar da ɗansa,
haka UBANGIJI Allahnku ke horar da ku.

[6] Ku kiyaye umarnan UBANGIJI Allahnku, kuna tafiya cikin hanyoyinsa, kuna kuma
girmama shi. [7] Gama UBANGIJI Allahnku yana fitar da ku zuwa cikin ƙasa mai kyau,
ƙasa mai rafuffuka da tafkunan ruwa, tare da maɓulɓulai masu gudu a kwari da
tuddai; [8] ƙasa mai alkama da sha'ir, inabi da ɓaure, rumman, man zaitun da zuma;
[9] ƙasa inda abinci ba zai yi ƙaranci ba, ba kuma za ku rasa kome ba; ƙasa ce inda
ƙarfe ne duwatsunta, ana kuma haƙar tagulla a tuddanta.

[10] Sa'ad da kuka ci, kuka ƙoshi, sai ku yabi UBANGIJI Allahnku saboda ƙasa mai
kyau da ya ba ku. [11] Ku yi hankali cewa ba ku manta da UBANGIJI Allahnku, har
ku kāsa kiyaye umarnansa, dokokinsa da ƙa'idodinsa da nake ba ku a wannan rana
ba. [12] To, sa'ad da kuka ci, kuka ƙoshi, sa'ad da kuka gina gidaje masu kyau, kuka
zauna, [13] sa'ad da kuma garkunanku na shanu da na tumaki suka ƙaru, azurfanku da
zinariyarku kuma suka ƙaru, sa'an nan dukan abin da kuke da shi ya haɓaka, [14] to,
sai ku lura, kada ku ɗaukaka kanku, har ku manta da UBANGIJI Allahnku, wanda ya
fitar da ku daga Masar, daga ƙasar bauta kuma. [15] Ya bishe ku cikin hamada mai
fāɗi, mai bantsoro, wannan busasshiyar ƙasa wadda ba ta da ruwa, ga macizai masu
dafi da kuma kunamai. Ya ba ku ruwa daga dutsen ƙanƙara. [16] Ya ba ku Manna don
ku ci a cikin hamada, wani abin da kakanninku ba su taɓa sani ba, don yă ƙasƙantar
yă kuma gwada ku, saboda yă yi muku alheri daga baya. [17] Wataƙila ku ce wa kanku,

"Ikona da ƙarfin hannuwana ne suka ba ni da wannan arziki." [18] Amma ku tuna da
Ubangiji Allahnku, gama shi ne wanda yake ba ku azanci na yin arziki, ta haka kuwa
ya tabbatar da alkawarinsa, wanda ya rantse wa kakanninku, kamar yadda yake a
yau.
[19] In kuka manta da Ubangiji Allahnku, kuka kuma bi waɗansu alloli, kuka yi
musu sujada, kuka kuma rusuna musu, to, a yau ina gargaɗe ku cewa tabbatacce za
a hallaka ku. [20] Kamar al'ummai da Ubangiji ya hallakar kafin ku, haka zai hallaka
ku, domin ba ku yi biyayya da muryar Ubangiji Allahnku ba.

# 9

*Ba don adalcin Isra'ila ba ne*

[1] Ku ji, ya Isra'ila. Kuna gab da haye Urdun, ku shiga, ku kuma kori al'ummai da
suka fi ku yawa, suka kuma fi ku ƙarfi, masu manyan biranen da suke da katangar da
suka yi tsaye zuwa sama. [2] Mutane ne masu ƙarfi, kuma dogaye, zuriyar Anakawa!
Ai, kun ji akan ce, "Wa zai iya tsayayya da Anakawa?" [3] Amma ku zauna da sani a
yau, cewa Ubangiji Allahnku, shi ne wanda ya ƙetare ya sha gabanku kamar wuta
mai cinyewa. Zai hallaka su, zai rinjaye su a gabanku. Za ku kore su, ku kuma hallaka
su nan da nan, yadda Ubangiji ya yi muku alkawari.
[4] Bayan Ubangiji Allahnku ya kore su a gabanku, kada ku faɗa a zuciyarku,
"Ubangiji ya kawo mu a nan, mu mallaki wannan ƙasa saboda adalcinmu ne." A'a,
saboda muguntar waɗannan al'umma ne ya sa Ubangiji ya kore su a gabanku. [5] Ba
domin adalci ko mutuncinku ba ne ya sa za ku mallaki ƙasarsu; sai dai saboda
muguntar al'umman nan ne ya sa Ubangiji Allahnku yana korinsu a gabanku don yǎ
cika abin da ya rantse wa kakanninku, wato, Ibrahim, Ishaku da Yaƙub. [6] Ku gane
wannan, cewa ba domin adalcinku ba ne ya sa Ubangiji Allahnku yana ba ku wannan
ƙasa mai kyau, ku mallaki, gama ku mutane masu taurinkai ne.

*Ɗan maraƙin zinariya*
*(Fitowa 32)*

[7] Ku tuna da wannan, kada kuma ku manta yadda kuka tsokane Ubangiji Allahnku,
har ya yi fushi a hamada. Daga ranar da kuka bar Masar har sai da kuka isa nan,
kuna ta tawaye wa Ubangiji. [8] A Horeb, kun tayar wa Ubangiji har ya yi fushin da
ya isa yǎ hallaka ku. [9] Sa'ad da na hau kan dutse don in karɓi allunan dutse, allunan
alkawarin da Ubangiji ya yi da ku, na zauna a kan dutse yini arba'in da dare arba'in;
ban ci abinci ba, ban sha ruwa ba. [10] Ubangiji ya ba ni alluna biyu wanda shi kansa
ya yi rubutu da yatsarsa. A kansu akwai dukan umarnan Ubangiji da an furta muku
a kan dutse a tsakiyar wuta, a ranar taron jama'a.
[11] A ƙarshen yini arba'in da dare arba'in ɗin, Ubangiji ya ba ni alluna biyu na
dutse, allunan alkawari. [12] Sa'an nan Ubangiji ya faɗa mini, "Sauka daga nan da
sauri, domin mutanenka waɗanda ka fitar da su daga Masar sun lalace. Sun juye da
sauri daga abin da na umarce su, suka kuma yi zubin gunki wa kansu."
[13] Sai Ubangiji ya ce mini, "Na ga mutanen nan, su masu taurinkai ne sosai! [14] Bar
ni kawai, in hallaka su, in kuma shafe sunansu daga ƙarƙashin sama. Zan kuwa yi
maka wata al'umma mafi ƙarfi da kuma masu yawa fiye da su."
[15] Saboda haka na juya, na sauko daga dutsen yayinda yake cin wuta. Allunan biyu
na alkawarin kuma suna a hannuwana.* [16] Sa'ad da na duba, sai na ga cewa kun yi
zunubi wa Ubangiji Allahnku; kun yi wa kanku gunkin da kuka yi zubi a siffar ɗan
maraƙi. Kun kauce da sauri daga hanyar da Ubangiji ya umarce ku. [17] Saboda haka
na ɗauko alluna biyun na jefar da su daga hannuwana, na farfashe su a idanunku.

* **9:15** Ko kuwa Kuma ina da alluna biyu na alkawarin tare da ni, ɗaya a kowane hannu

[18] Sai nan da nan kuma na fāɗi rubda ciki a gaban UBANGIJI, yini arba'in da dare
arba'in; ban ci ba, ban sha ba, kamar yadda dā na yi, duka saboda zunubin da kuka
aikata a gaban UBANGIJI. Ta haka kuka tsokane shi don yă yi fushi. [19] Na ji tsoron
fushi da hasalar UBANGIJI, gama ya yi fushin da ku da ya isa yă hallaka ku. Amma
na yi roƙo a lokacin, UBANGIJI kuwa ya saurare ni. [20] UBANGIJI ya yi fushi sosai da
Haruna, har ya yi niyya yă hallaka shi, amma a wannan lokaci, na yi addu'a saboda
Haruna shi ma. [21] Sa'an nan na ɗauki kayan zunubin da kuka yi, wato, gunkin ɗan
bijimi, na ƙone shi da wuta, na farfashe shi, na niƙa shi liƀis, sai da ya zama kamar
ƙura mai laushi, na zubar da ƙurar a cikin ruwan rafin da yake gangarowa daga
dutse.
[22] Kun kuma sa UBANGIJI ya yi fushi a Tabera, a Massa da kuma a Kibrot Hatta'awa.
[23] Sa'ad da UBANGIJI ya aike ku daga Kadesh Barneya ya ce, "Ku haura ku mallaki
ƙasar da na ba ku." Amma kuka yi tawaye ga umarnin UBANGIJI Allahnku. Ba ku
amince da shi, ko ku yi masa biyayya ba. [24] Kun yi ta tawaye wa UBANGIJI tun ran da
na san ku.
[25] Na kwanta rubda ciki a gaban UBANGIJI waɗannan yini arba'in da dare arba'in
domin UBANGIJI ya ce zai hallaka ku. [26] Na yi addu'a ga UBANGIJI na ce, "Ya UBANGIJI
Mai Iko Duka, kada ka hallaka mutanenka, gādon kanka, da ka fansa ta wurin ikonka
mai girma, ka kuma fitar da su daga Masar da hannu mai ƙarfi. [27] Ka tuna da bayinka
Ibrahim, Ishaku da Yaƙub. Kada ka kula da taurinkan, mugunta da kuma zunubin
wannan mutane. [28] In ba haka ba, ƙasar da ka fitar da mu, za tă ce, 'Domin UBANGIJI
bai iya kai su cikin ƙasar da ya yi musu alkawari ba ne, kuma domin ya ƙi su, shi ya
sa ya fitar da su ya kashe su a hamada.' [29] Amma su mutanenka ne, gādonka da ka
fitar ta wurin ikonka mai girma, da kuma hannunka mai ƙarfi."

# 10

### *Alluna kamar na farko*
*(Fitowa 34.1-10)*

[1] A lokacin UBANGIJI ya ce mini, "Ka sassaƙa alluna biyu na dutse kamar na farko,
ka haura wurina a kan dutse. Ka kuma yi akwatin katako.* [2] Ni kuwa zan yi rubutu
a kan allunan nan biyu, kalmomin da suke a alluna na farko, waɗanda ka farfashe.
Za a ajiye su a cikin akwatin."
[3] Sai na yi akwatin da itacen ƙirya, na kuma sassaƙa alluna biyu na dutse kamar na
farko, sai na haura dutse da alluna biyun a hannuwana. [4] UBANGIJI kuwa ya sāke yin
rubutu a waɗannan alluna abin da ya rubuta a allunan farko, wato, Dokoki Goma da
ya furta a kan dutse a tsakiyar wuta, a ranar da mutane suka taru. Sai UBANGIJI ya
ba ni su. [5] Sa'an nan na sauko daga dutsen, na kuma ajiye allunan a cikin akwatin
da na yi, yadda UBANGIJI ya umarce ni, kuma suna can a yanzu.
*(Kidaya 20.22-29)*
[6] (Isra'ilawa suka kama hanya daga rijiyoyin Beyerot Bene Ya'akan zuwa Mosera.
A can Haruna ya rasu, aka kuma binne shi. Sai Eleyazar ɗansa ya gāje shi a matsayin
firist. [7] Daga can suka tashi zuwa Gudgoda, daga Gudgoda kuma suka tafi Yotbata,
ƙasa mai rafuffukan ruwa. [8] A lokacin UBANGIJI ya keɓe kabilar Lawi don su riƙa
ɗaukar akwatin alkawarin UBANGIJI, su tsaya a gaban UBANGIJI, su riƙa yin masa
hidima, su kuma sa albarka a cikin sunansa, yadda suke yi har wa yau. [9] Shi ya sa
Lawiyawa ba su da rabo, ko gādo a cikin 'yan'uwansu; UBANGIJI ne gādonsu yadda
UBANGIJI Allahnku ya faɗa musu.)
*(Fitowa 34.9,10,27-29)*

* **10:1** Wato, akwatin alkawari

10 To, na kasance a kan dutse yini arba'in da dare arba'in kamar yadda dā na yi
da farko. UBANGIJI kuwa ya saurare ni a wannan lokaci kuma. Ba nufinsa ba ne
yă hallaka ku. 11 UBANGIJI ya ce mini, "Ka sauka, ka jagoranci mutanen a hanyarsu,
domin su shiga, su kuma mallaki ƙasar da na rantse wa kakanninsu, zan ba su."

*Ku ji tsoron UBANGIJI*

12 Yanzu fa, ya Isra'ila, mene ne UBANGIJI Allahnku yake so a gare ku, in ba ku ji
tsoron UBANGIJI Allahnku, ku yi tafiya cikin hanyoyinsa, ku ƙaunace shi, ku bauta
wa UBANGIJI Allahnku da dukan zuciyarku da kuma dukan ranku, 13 ku kuma kiyaye
umarnan UBANGIJI da kuma ƙa'idodinsa da nake ba ku a yau don amfaninku ba?
14 Sammai, har da sama sammai, da duniya, da kome da yake cikinta na UBANGIJI
Allahnku ne. 15 Duk da haka UBANGIJI ya ƙaunaci kakanninku, ya kuma zaɓe ku,
ku zuriyarsu, a bisa dukan al'ummai, yadda yake a yau. 16 Saboda haka sai ku kame
zukatanku, kada ku ƙara yin taurinkai. 17 Gama UBANGIJI Allahnku ne Allahn alloli da
Ubangijin iyayengiji, Allah mai girma, mai ƙarfi da kuma mai banrazana, wanda ba
ya sonkai, ba ya cin hanci. 18 Yakan tsare marayu da gwauraye, yana ƙaunar baƙon
da yake zama a cikinku, yana ba su abinci da tufafi. 19 Sai ku ƙaunaci baƙi, gama dā
ku ma baƙi ne a ƙasar Masar. 20 Ku ji tsoron UBANGIJI Allahnku, ku kuma bauta masa.
Ku manne masa, ku kuma yi rantsuwarku da sunansa. 21 Shi ne abin yabonku; shi
ne Allahnku, wanda ya aikata muku waɗancan manya abubuwa banmamaki masu
banrazanar da kuka gani da idanunku. 22 Kakanninku da suka gangara zuwa Masar,
su saba'in ne, yanzu kuwa UBANGIJI Allahnku ya sa kuka ƙaru, kuka zama kamar
taurari a sama.

# 11

*Ku ƙaunaci ku kuma yi biyayya ga UBANGIJI*

1 To, sai ku ƙaunaci UBANGIJI Allahnku, kullum ku kuma kiyaye abubuwan da yake
bukata, ku kiyaye ƙa'idodinsa, dokokinsa da kuma umarnansu. 2 Ku tuna a yau,
cewa 'ya'yanku ba su ne suka gani suka kuma ɗanɗana horon UBANGIJI Allahnku ba;
ba su suka gani girmansa, hannunsa mai ƙarfi, hannunsa mai iko; 3 alamun da ya
aikata da abubuwan da ya yi a cikin Masar, ga Fir'auna sarkin Masar da kuma ga
dukan ƙasarsa ba; 4 ba su suka gani abin da ya yi wa mayaƙan Masar, da dawakansu
da keken yaƙinsu, yadda ya sha kansu da ruwan Jan Teku yayinda suke bin ku, da
yadda UBANGIJI ya hallaka su ƙaƙaf ba. 5 Ba 'ya'yanku ba ne suka gani abin da ya
yi dominku a hamada har sai da kuka kai wannan wuri ba, 6 ba su ba ne suka gani
abin da ya yi ga Datan da Abiram, 'ya'yan Eliyab mutumin Ruben, sa'ad da ƙasa ta
buɗe bakinta a tsakiyar dukan Isra'ila ta haɗiye su tare da gidajensu, tentunansu da
kowane abu mai rai da yake nasu ba. 7 Amma idanunku ne suka ga dukan waɗannan
manyan abubuwan da UBANGIJI ya yi.
8 Saboda haka sai ku kiyaye dukan umarnan da nake ba ku a yau, don ku sami
ƙarfin da za ku shiga, ku kuma karɓi ƙasar da kuke haye Urdun ku mallaka, 9 domin
kuma ku yi tsawon rai a ƙasar da UBANGIJI ya rantse wa kakanninku zai ba su da
zuriyarsu, ƙasa mai zub da madara da zuma. 10 Kasar da kuke shiga, ku karɓa, ba
kamar ƙasar Masar ba ce, inda kuka fito, inda kuka shuka iri, ku yi ta zuwa kuna
banruwa kamar lambu. 11 Amma ƙasar da kuke haye Urdun ku mallaki, ƙasa ce ta
duwatsu da kwaruruka wadda ruwan sama ne yake jiƙe ta. 12 Kasa ce da UBANGIJI
Allahnku yake lura da ita; idanun UBANGIJI Allahnku yana a kai daga farkon shekara
har zuwa ƙarshenta.
13 Saboda haka in kun yi biyayya ga umarnan da nake ba ku a yau cikin aminci,
kuna ƙaunaci UBANGIJI Allahnku, kuna kuma bauta masa da dukan zuciyarku da

kuma dukan ranku, [14] sai in aika da ruwan sama a ƙasarku a lokacinsa, ruwan
saman bazara da kuma na kaka, don ku tattara hatsinku, sabon inabinku da kuma
manku. [15] Zan tanadar da ciyawa a filaye don shanunku, za ku ci, ku kuma ƙoshi.

[16] Ku yi hankali, kada a ruɗe ku har ku bauta wa alloli, ku kuma yi musu sujada,
[17] don kada fushin UBANGIJI yă ƙuna a kanku, yă rufe sammai, ku rasa ruwa, ƙasa
kuma ta kāsa ba da amfaninta, da haka za ku murmutu nan da nan a kyakkyawar
ƙasar da UBANGIJI yake ba ku. [18] Saboda haka, sai ku riƙe waɗannan kalmomina
gam a zukatanku da ranku; ku ɗaura su kamar alama a hannuwanku, da goshinku.
[19] Ku koyar da su ga 'ya'yanku, ku yi ta haddace su, sa'ad da kuke zaune a gida, da
sa'ad da kuke tafiya, sa'ad da kuke kwance, da sa'ad da kuka tashi. [20] Ku rubuta su
a kan madogaran ƙofofin gidajenku, da a kan ƙofofinku, [21] saboda kwanakinku da
kwanakin 'ya'yanku su yi tsawo a ƙasar da UBANGIJI ya rantse zai ba wa kakanninku,
muddin sama tana bisa duniya.

[22] In kuka lura, kuka kuma kiyaye dukan umarnai da nake ba ku, ku ƙaunaci
UBANGIJI Allahnku, ku yi tafiya a hanyoyinsa, ku kuma riƙe shi gam, [23] UBANGIJI zai
kori dukan waɗannan al'ummai a gabanku, za ku kuma kore al'umman da suka fi ku
yawa da ƙarfi. [24] Duk inda tafin ƙafanku ya taka, zai zama naku; iyakarku zai kama
daga hamadan Lebanon da kuma daga Kogin Yuferites zuwa Bahar Rum.* [25] Babu
mutumin da zai iya tsayayya da ku. UBANGIJI Allahnku, zai sa razana da tsoronku a
dukan ƙasar, a duk inda kuka tafi, kamar yadda ya alkawarta muku.

[26] Ga shi, a yau, ina sa a gabanku albarka da kuma la'ana, [27] albarka in kun yi
biyayya da umarnan UBANGIJI Allahnku, da nake ba ku; [28] la'ana in ba ku yi biyayya
da umarnan UBANGIJI Allahnku, kuka kuma juya daga hanyar da na umarce ku, ta
wurin bin waɗansu alloli, waɗanda ba ku sani ba. [29] Sa'ad da UBANGIJI Allahnku
ya kawo ku cikin ƙasar da za ku shiga ku ci gādonta, sai ku yi shelar albarkun nan
a dutsen Gerizim, ku kuma yi na la'ana a dutsen Ebal. [30] Waɗannan duwatsu biyu
suna a hayin Urdun, yamma da hanya a ƙasar Kan'aniyawa mazaunan Araba, kusa
da Gilgal wajajen manyan itatuwan More. [31] Kuna gab da ƙetare Urdun fa, ku shiga,
ku kuma mallaki ƙasar da UBANGIJI Allahnku yake ba ku. Sa'ad da kuka karɓe ta,
kuka kuma zauna a can, [32] ku tabbata kun yi biyayya da dukan ƙa'idodi, da kuma
dokokin da nake sawa a gabanku a yau.

# 12

*Wuri ɗaya kaɗai don yin sujada*

[1] Waɗannan su ne ƙa'idodi da kuma dokokin da za ku lura, ku kuma kiyaye a ƙasar
da UBANGIJI, Allahn kakanninku, yake ba ku don ku ci gādonta, muddin kuna zama
a ƙasar. [2] Ku hallaka dukan wuraren da al'umman da kuke kora suke yi wa allolinsu
sujada, a kan duwatsu masu tsawo, da a kan tuddai, da kuma ƙarƙashin kowane itace
gaba ɗaya. [3] Ku rurrushe bagadansu, ku farfashe keɓaɓɓun duwatsunsu, ku kuma
ƙone ginshiƙan Asheransu da wuta; ku yayyanka gumakan allolinsu, ku kuma shafe
sunayensu daga waɗannan wurare.

[4] Ba za ku yi wa UBANGIJI Allahnku sujada a hanyar da suke yi ba. [5] Amma sai ku
nemi wurin da UBANGIJI Allahnku zai zaɓa daga cikin dukan kabilanku, inda zai sa
Sunansa, yă mai wurin mazauninsa. A wannan wuri ne za ku tafi; [6] a can ne kuma
za ku kawo hadayun ƙonawa da sadakoki, zakkarku da kyautai na musamman, da
abin da kuka yi alkawari za ku bayar, da hadayunku na yardar rai, da kuma 'ya'yan
farin garkunanku na shanu da na tumaki. [7] A can, a gaban UBANGIJI Allahnku, ku da

* **11:24** Wato, Mediterraniyan.

iyalanku za su ci, su kuma yi farin ciki a kome da kuka sa hannunku a kai, domin
UBANGIJI Allahnku zai albarkace ku.

8 Kada ku yi kamar yadda muke yi a nan yau, yadda kowa yake yin abin da ya
ga dama. 9 Gama ba ku kai wurin hutawa wanda UBANGIJI Allahnku zai ba ku gādo
ba tukuna. 10 Amma sa'ad da kuka haye Urdun, kuka zauna a ƙasar da UBANGIJI
Allahnku yake ba ku ita gādo, zai kuwa ba ku hutu daga dukan abokan gābanku da
suke kewaye da ku, kuka sami zaman lafiya, 11 sai ku kai dukan abin da na umarce
ku ku kai, wato, hadayu na ƙonawa, da sadakokinku, da zakkarku, da hadayunku
na ɗagawa, da hadayunku na alkawarin da kuka yi wa UBANGIJI a wurin da UBANGIJI
Allahnku ya zaɓa yă sa sunansa. 12 A can kuma za ku yi farin ciki a gaban UBANGIJI
Allahnku, ku da 'ya'yanku maza da mata, da bayinku maza da mata, da kuma
Lawiyawa daga biranenku, waɗanda ba a ba su rabo ba, ba su kuma da gādo na
kansu. 13 Ku kula fa kada ku miƙa hadayun ƙonawa a wani wurin da kuka ga dama.
14 Ku miƙa su kawai a wurin da UBANGIJI zai zaɓa a cikin ɗaya daga kabilanku, a can
za ku yi kowane abin da na umarce ku.

15 Amma kwa iya yanka nama ku ci a garuruwanku, a duk lokacin da ranku yake
so, kamar yadda ake yi da gada ko barewa, bisa ga albarkar da UBANGIJI Allahnku
yake sa muku. Marar tsarki da mai tsarki, duka za ku iya ci. 16 Amma kada ku ci jini,
ku zubar da shi a ƙasa kamar ruwa. 17 Kada ku ci zakkar hatsi, da na sabon inabi,
da kuma na mai a biranenku, ko kuwa na 'ya'yan fari na garkunanku na shanu da
na tumaki, ko kuwa duk wani abin da kuka yi alkawari za ku bayar, ko hadayunku
na yardar rai, ko kyautai na musamman. 18 A maimakon haka, sai ku ci su a gaban
UBANGIJI Allahnku a wurin da UBANGIJI Allahnku ya zaɓa, da ku da 'ya'yanku maza
da mata, da bayinku maza da mata, da kuma Lawiyawa daga biranenku, ku kuwa yi
farin ciki a gaban UBANGIJI Allahnku a kowane abin da kuka sa hannunku. 19 Ku yi
hankali, kada ku manta da Lawiyawa, muddin kuna zaune a ƙasarku.

20 Sa'ad da UBANGIJI Allahnku ya fadada iyakarku kamar yadda ya yi muku
alkawari, kuka kuma ji marmarin nama, kuka kuma ce, "Muna so mu ci nama,"
to, za ku iya cin yadda kuke so. 21 In wurin da UBANGIJI Allahnku ya zaɓa don
yă sa Sunansa yana da nisa sosai daga inda kuke, za ku iya yankan dabbobi daga
garkunanku na shanu da na tumakin da UBANGIJI ya ba ku, kamar yadda na umarce
ku, a cikin biranenku kuma za ku iya ci, yadda kuke so. 22 Ku ci su yadda akan ci
barewa ko mariri. Marar tsarki da mai tsarki, za ku iya ci. 23 Amma ku tabbata ba ku
ci jinin ba, domin jini ne rai, ba kuwa za ku ci rai cikin naman ba. 24 Ba za ku ci jini
ba, ku zubar da shi a ƙasa kamar ruwa. 25 Kada ku ci shi, don ku zauna lafiya, da ku
da 'ya'yanku bayanku, gama za ku riƙa aikata abin da yake daidai a gaban UBANGIJI.

26 Amma ku ɗauki abubuwa masu tsarki, da kuma duk abin da kuka yi alkawari
za ku bayar, ku tafi inda UBANGIJI ya zaɓa. 27 Ku miƙa hadayunku na ƙonawa a
bagaden UBANGIJI Allahnku, da naman da kuma jinin. Dole a zub da jinin hadayunku
a gindin bagaden UBANGIJI Allahnku, amma za ku iya cin naman. 28 Ku yi hankali,
ku yi biyayya da dukan waɗannan umarnan da nake ba ku, da kuma 'ya'yanku, don
ku zauna lafiya, da ku da 'ya'yanku a bayanku, gama za ku riƙa aikata abin da yake
daidai da kuma yake mai kyau a gaban UBANGIJI Allahnku.

29 UBANGIJI Allahnku zai kawar muku da al'umman nan da kuke niyyar shiga cikin
ƙasarsu don ku kore su, bayan kuka kore su, kuka kuma zauna a ƙasarsu, 30 to,
sai ku lura, kada ku jarrabtu ku kwaikwaye su bayan da an riga an shafe su daga
gabanku, kada ku tambayi kome game da allolinsu, kuna cewa, "Yaya waɗannan
al'ummai suke bauta wa allolinsu? Mu ma za mu yi kamar yadda suka yi." 31 Ba za
ku yi wa UBANGIJI Allahnku sujada a hanyar da suke yi ba, gama a cikin yin sujada wa

allolinsu, sun yi dukan abubuwan banƙyaman da Ubangiji yake ƙi. Har ma sukan
ƙone 'ya'yansu maza da mata a wuta a matsayin hadayu.
32 Ku lura, ku aikata dukan abin da na umarce ku; kada ku ƙara, kada ku rage daga
cikin.

## 13

*Bautar waɗansu alloli*
1 In wani annabi ko mai mafarkai, ya bayyana a cikinku, ya kuma yi muku shelar
wata alama mai banmamaki ko al'ajabi, 2 in kuwa alamar, ko al'ajabin da annabin
ya yi faɗin ya faru, ya kuma ce, "Bari mu bi waɗansu alloli (allolin da ba ku sani
ba) mu kuma yi musu sujada," 3 kada ku saurari kalmomin wannan annabi ko mai
mafarki. Ubangiji Allahnku yana gwada ku ne don yă sani ko kuna ƙaunarsa da
dukan zuciyarku da kuma dukan ranku. 4 Ubangiji Allahnku ne za ku bi, shi ne
kuma za ku girmama. Ku kiyaye umarnansa, ku kuma yi masa biyayya; ku bauta
masa, ku kuma manne masa. 5 Dole a kashe wannan annabi ko mai mafarki, domin
ya yi wa'azin tawaye ga Ubangiji Allahnku, wanda ya fitar da ku daga Masar, ya
fanshe ku daga ƙasar bauta; gama annabin nan ya yi ƙoƙari yă juye daga hanyar da
Ubangiji Allahnku ya umarce ku, ku bi. Dole ku fid da mugu daga cikinku.
6 In ɗan'uwanka, ko ɗanka, ko 'yarka, ko matar da kake ƙauna, ko abokinka na
kusa, a ɓoye ya ruɗe ka, yana cewa, "Mu je mu yi wa waɗansu alloli sujada" (allolin
da ko kai, ko kakanninka ba su sani ba, 7 allolin mutanen kewayenku, ko na kusa, ko
na nisa, daga wannan ƙarshen ƙasar zuwa wancan), 8 kada ka yarda da shi, kada ma
ka saurare shi. Kada ka ji tausayinsa. Kada ka haƙura da shi, ko ka tsare shi. 9 Dole ka
kashe shi. Dole hannunka yă zama na farko a kisansa, sa'an nan hannuwan sauran
dukan mutane. 10 Ku jajjefe shi da duwatsu har sai ya mutu, domin ya yi ƙoƙari yă
juye ku daga Ubangiji Allahnku, wanda ya fitar da ku daga Masar, daga ƙasar bauta
kuma. 11 Sa'an nan dukan Isra'ila za su ji su kuma tsorata, babu kuma wani a cikinku
da zai ƙara yin irin wannan mugun abu.
12 In kuka ji an yi magana a kan wani daga cikin biranen da Ubangiji Allahnku yake
ba ku ku zauna a ciki 13 cewa mugaye sun taso a cikinku, suna rikitar da mutane a
birni, suna cewa, "Mu je mu yi wa waɗansu alloli sujada" (allolin da ba ku sani ba),
14 to, sai ku bincike labarin sosai a hankali. In kuwa gaskiya ne, an kuma tabbatar
wannan abin ƙyama ya faru a cikinku, 15 dole a karkashe dukan waɗanda suke zama
a wannan birni da takobi. Ku hallaka su ƙaƙaf, ku karkashe mutanen birnin da kuma
dabbobinsa. 16 Ku tattara dukan ganimar birnin a tsakiyar gari, ku ƙone birnin da
kuma ganimar ƙurmus a matsayin hadaya ta ƙonawa ga Ubangiji Allahnku. Birnin
zai kasance kufai har abada, kada a sāke gina shi. 17 Ba za a iske wani daga cikin
abubuwan nan da aka haramta a hannuwanku ba, saboda Ubangiji yă juya daga
fushinsa mai ƙuna, yă nuna jinƙai, yă ji tausayinku, yă kuma ƙara yawanku, kamar
yadda ya alkawarta da rantsuwa ga kakanninku, 18 domin kun yi biyayya da Ubangiji
Allahnku, kuna kiyaye dukan umarnan da nake ba ku a yau, kuna kuma aikata abin
da yake daidai a idanunsa.

## 14

*Abinci mai tsabta da marar tsabta*
1 Ku 'ya'yan Ubangiji Allahnku ne. Kada ku yi wa kanku zāne, ko ku yi wa kanku
aski irin da akan bar sanƙo, saboda wanda ya mutu, 2 gama ku jama'a ce mai tsarki
ga Ubangiji Allahnku. Daga dukan mutane a fuskar duniya, Ubangiji ya zaɓe ku, ku
zama abin mallakarsa.
*(Firistoci 11.1-47)*

[3] Kada ku ci wani haramtaccen abu. [4] Waɗannan su ne dabbobin da za ku iya ci,
saniya, tunkiya, akuya, [5] mariri, barewa, mariya, makwarna, mazo, gada da kuma
tunkiyar dutse.* [6] Za ku iya cin duk dabbar da take da rababben kofato, wadda
kuma take sāke tona abin da suka riga suka haɗiye. [7] Amma, cikin waɗanda suke
sāke tona abin da suka riga suka haɗiye ɗin, ko suke da rababben kofato, ba za ku ci
raƙumi, zomo ko rema ba. Ko da yake suna sāke tona abin da suka riga suka haɗiye,
suna kuma da rababben kofato, su ɗin marar tsarki ne gare ku. [8] Alade ma marar
tsarki ne; ko da yake yana da rababben kofato, shi ba ya sāke tona abin da ya riga
ya haɗiye. Ba za ku ci namansu ko ku taɓa gawarsu ba.
[9] Cikin dukan halittun da suke cikin ruwa, za ku iya cin duk wani da yake da ƙege
da ɓamɓaroki. [10] Amma duk wani abin da ba shi da ƙege da ɓamɓaroki, ba za ku ci
ba; gama marar tsarki ne gare ku.
[11] Za ku iya cin kowane tsuntsu mai tsabta. [12] Amma waɗannan ba za ku ci ba,
gaggafa, ungulu, ungulun kwakwa, [13] duki, buga zaɓi, kowace irin shirwa, [14] kowane
irin hankaka, [15] jimina, ƙururu, bubuƙuwa, kowane irin shaho, [16] da mujiya, da
babbar mujiya, ɗuskwi, [17] kwasakwasa, ungulu, da babba da jaka, [18] zalɓe, kowane
irin jinjimi, katutu, da kuma jamage.
[19] Dukan 'yan ƙwari masu fikafikai masu rarrafe, haram ne a gare ku, kada ku ci
su. [20] Amma duk wata halitta mai fikafikai mai tsabta ce, za ku iya ci.
[21] Kada ku ci abin da kun samu ya riga ya mutu. Za ku iya ba wa baren da yake
zama a cikin wani daga biranenku, zai kuwa iya cinsa, ko kuwa za ku iya sayar da
shi wa baƙo. Amma ku jama'a ce mai tsarki ga UBANGIJI Allahnku.
Kada ku dafa ɗan akuya a cikin madara mamansa.

*Zakka*

[22] Ku tabbata kun keɓe kashi ɗaya bisa goma na amfanin gonakinku kowace
shekara. [23] Ku ci zakkar hatsinku, da na sabon ruwan inabinku, da na manku,
da kuma na 'ya'yan fari na garkunanku na shanu da na tumaki a gaban UBANGIJI
Allahnku, a wurin da ya zaɓa a matsayin mazauni don Sunansa, don ku koyi girmama
UBANGIJI Allahnku kullum. [24] Amma in wurin nan yana da nisa sosai, UBANGIJI
Allahnku kuma ya albarkace ku, ba za ku kuwa iya riƙe zakkarku ba (Saboda wurin
da UBANGIJI ya zaɓa yă sa Sunansa ya yi nisa sosai), [25] to, sai ku sayar da zakkar, ku
tafi da kuɗin wurin da UBANGIJI Allahnku ya zaɓa. [26] Yi amfani da kuɗin ku saya duk
abin da kuke so, ko shanu, ko tumaki, ko ruwan inabi, ko dai wani abin shan da ya yi
tsami, ko kuwa duk abin da kuke so. Sai ku da gidanku, ku ci a can, a gaban UBANGIJI
Allahnku, ku kuma yi farin ciki. [27] Kada dai ku manta da Lawiyawan da suke zama
a biranenku, gama ba su da rabo, ko gādo na kansu.
[28] A ƙarshen kowace shekara uku, ku kawo dukan zakkarku na amfanin gona na
wannan shekara, ku ajiye su a cikin birane, [29] saboda Lawiyawa (waɗanda ba su
da rabo ko gādo na kansu) da baƙo, da marayu, da kuma gwauraye, waɗanda suke
zama a biranenku, su zo su ci su ƙoshi, ta haka UBANGIJI Allahnku zai albarkace ku
cikin dukan ayyukan hannuwanku.

# 15

*Shekara ta yafe bashi*
*(Firistoci 25.1-7)*

[1] A ƙarshen kowace shekara ta bakwai, dole ku yafe basusuwan da kuke bi. [2] Ga
yadda za ku yafe basusuwan, kowane mai bin bashi, yă yafe bashin da yake bin
ɗan'uwansa mutumin Isra'ila. Ba zai bukaci mutumin Isra'ila wanda yake ɗan'uwa

* **14:5** Ainihin irin waɗansu tsuntsaye da dabbobi a wannan surar ba tabbatattu ba ne.

yă biya shi bashi ba, gama an yi shelar lokacin da UBANGIJI ya ajiye na yafe bashi.
3 Za ku iya nemi baƙo yă biya ku bashin da kuke binsa, amma dole ku yafe duk
wani bashin da kuke bin ɗan'uwa. 4 Amma bai kamata a sami matalauci a cikinku
ba, gama UBANGIJI Allahnku zai albarkace ku a ƙasar da yake ba ku, ku mallaka a
matsayin gādo, 5 in dai kun yi cikakken biyayya ga UBANGIJI Allahnku, kuka kuma
lura, kuna kiyaye dukan waɗannan umarnan da nake ba ku yau. 6 Gama UBANGIJI
Allahnku zai albarkace ku kamar yadda ya yi alkawari, za ku kuma ba al'ummai
masu yawa bashi, amma ba za ku karɓa bashi daga wurin wani ba. Za ku yi mulkin
al'ummai masu yawa, babu wata kuwa da za tă yi mulkinku.

7 In akwai matalauci a cikin 'yan'uwanku, a duk wani daga cikin biranen da
UBANGIJI Allahnku yake ba ku, kada ku taurara zuciya, ko ku ƙi saki hannu ga
ɗan'uwanku matalauci. 8 A maimakon haka ku bayar hannu sake, ku kuma ba shi
bashi gwargwadon abin da yake bukata a sauƙaƙe. 9 Ku yi hankali kada ku riƙe
wannan mugun tunani cewa, "Shekara ta bakwai, shekarar yafewar basusuwa, ta
yi kusa," har ku nuna mugun nufi ga ɗan'uwa mabukaci, ku ƙi ba shi wani abu.
Zai yi kuka ga UBANGIJI a kanku, abin kuwa zai zama laifi a kanku. 10 Ku bayar
hannu sake gare shi, ku kuma yi haka ba tare da gunaguni ba; saboda wannan fa
UBANGIJI Allahnku zai albarkace ku a cikin dukan aikinku, da kuma kome da kuka
sa hannunku a kai. 11 Kullum za ku kasance da matalauta a ƙasar. Saboda haka na
umarce ku ku bayar hannu sake ga 'yan'uwa da kuma matalauta, da masu bukata a
ƙasarku.

### *Ba da 'yanci ga bayi*
### *(Fitowa 21.1-11)*

12 In ɗan'uwa mutumin Ibraniyawa, namiji ko ta mace, ya sayar da kansa gare
ka, ya kuma bauta maka shekaru shida, a shekara ta bakwai dole ka 'yantar da shi.
13 Sa'ad da kuka sake shi, kada ku bar shi yă tafi hannu wofi. 14 Ku ba shi kyautai
hannu sake daga tumakinku, daga masussukarku, da kuma daga wurin matsewar
inabinku. Ku ba shi yadda UBANGIJI Allahnku ya albarkace ku. 15 Ku tuna, dā ku
bayi ne a Masar, UBANGIJI Allahnku kuma ya fisshe ku. Shi ya sa nake ba ku wannan
umarni a yau.

16 Amma in bawanka ya ce maka, "Ba na so in bar ka," saboda yana ƙaunarka da
iyalinka, ya kuma fiye masa yă zauna da kai, 17 sai ka ɗauki basilla ka huda kunnensa
a bakin ƙofa, zai kuwa zama bawanka dukan rayuwarsa. Ka yi haka ma wa baiwarka.

18 Sa'ad da kuka 'yantar da shi kada ku damu, gama shekara shida ya yi muku
bauta wadda ta ninka ta ɗan ƙodago. UBANGIJI Allahnku kuwa zai albarkace ku a
kome da kuke yi.

### *'Ya'yan fari na dabbobi*
### *(Firistoci 27.26,27; Kidaya 18.15-18)*

19 Ku keɓe wa UBANGIJI Allahnku kowane ɗan fari na garkenku na shanu, da na
tumaki. Kada ku sa ɗan fari na shanunku aiki, kada kuma ku aske gashin ɗan fari na
tumakinku. 20 Kowace shekara, kai da iyalinka za ku ci su a gaban UBANGIJI Allahnku,
a wurin da ya zaɓa. 21 In dabbar tana da lahani, gurguntaka ko makantaka, ko kuwa
tana da wani mugun lahani, kada ku miƙa ta ga UBANGIJI Allahnku. 22 Sai ku ci a
cikin biranenku. Mutum marar tsabta da mai tsabta zai iya ci kamar yadda ake yi da
barewa ko mariri. 23 Amma kada fa ku ci jinin, ku zubar da shi a ƙasa kamar ruwa.

## 16

### *Bikin Ketarewa*
### *(Fitowa 12.1-20; Firistoci 23.4-8)*

1 Ku kiyaye watan Abib, ku kuma yi shagalin Bikin Ketarewar UBANGIJI Allahnku,
domin a watan Abib ne ya fitar da ku daga Masar da dad dare. 2 Ku miƙa 'yar dabba
daga cikin garkenku na tumaki, ko na shanu a matsayin Bikin Ketarewa ga UBANGIJI
Allahnku a wurin da UBANGIJI zai zaɓa a matsayin mazauni don Sunansa. 3 Kada
ku ci shi da burodin da aka yi da yisti, kwana bakwai za ku ci burodi marar yisti,
burodi ne na wahala, gama kun bar Masar da gaggawa, saboda haka dukan kwanakin
rayuwarku za ku tuna da lokacin da kuka fita daga Masar. 4 Kada a iske yisti a cikin
mallakarku a dukan ƙasarku har kwana bakwai. Kada ku bar wani nama na hadayar
da kuka yi a yammancin ranar farko, yǎ kwana har safe.
5 Kada ku miƙa hadayar Bikin Ketarewa a wani garin da UBANGIJI Allahnku yake
ba ku, 6 sai dai a wurin da ya zaɓa yǎ zama mazauni don Sunansa. A can za ku miƙa
hadayar Bikin Ketarewa da yamma, sa'ad da rana tana fāɗuwa, a ranar tunawa
da fitowarku daga Masar. 7 Ku gasa shi, ku kuma ci a wurin da UBANGIJI Allahnku
ya zaɓa. Sa'an nan da safe, ku dawo cikin tentunanku. 8 Kwana shida za ku ci
burodi marar yisti, a rana ta bakwai kuma sai ku yi taro ga UBANGIJI Allahnku, a
cikin wannan rana ba za ku yi kowane irin aiki ba.

*Bikin Makoni*
*(Fitowa 34.22; Firistoci 23.15-21)*
9 Ku ƙirga makoni bakwai, wato, ku fara ƙirga mako bakwai ɗin daga lokacin da
kuka sa lauje don ku yanke hatsinku da suke tsaye. 10 Sa'an nan ku yi shagalin Bikin
Makoni ga UBANGIJI Allahnku, ta wurin ba da hadaya ta yardar rai daidai da albarkun
da UBANGIJI Allahnku ya yi muku. 11 Ku kuma yi farin ciki a gaban UBANGIJI Allahnku
a wurin da ya zaɓa a matsayin mazauni don Sunansa, da ku da 'ya'yanku maza da
mata, da bayinku maza da mata, da Lawiyawan cikin biranenku, har ma da baƙi, da
marayu, da kuma gwaurayen da suke zama a cikinku. 12 Ku tuna fa, dā ku bayi ne a
Masar, sai ku lura, ku bi waɗannan ƙa'idodi.

*Bikin tabanakul*
*(Firistoci 23.33-43; Kidaya 29.12-38)*
13 Ku yi shagalin Bikin Tabanakul har kwana bakwai, bayan kuka gama tattara
amfanin gona daga masussukarku da kuma daga wuraren matsin inabinku. 14 Ku yi
farin ciki a Bikinku, da ku da 'ya'yanku maza da mata, da bayinku maza da mata, da
Lawiyawa, da baƙi, da marayu, da kuma gwaurayen da suke zama a cikin biranenku.
15 Kwana bakwai za ku yi shagalin Bikin ga UBANGIJI Allahnku a wurin da ya zaɓa.
Gama UBANGIJI Allahnku zai albarkace ku a cikin dukan girbinku da kuma cikin
dukan aikin hannuwanku, farin cikinku kuwa zai cika.
*(Fitowa 23.14-17)*
16 Sau uku a shekara dukan maza su bayyana a gaban UBANGIJI Allahnku a wurin da
ya zaɓa; a Bikin Burodi Marar Yisti, da a Bikin Makoni, da kuma a Bikin Tabanakul.
Babu wani da zai bayyana a gaban UBANGIJI hannu wofi. 17 Dole kowannenku yǎ
kawo kyauta daidai yadda UBANGIJI Allahnku ya albarkace shi.

*Alƙalai*
18 Ku naɗa alƙalai da shugabanni don kowace kabila, a kowane birnin da UBANGIJI
Allahnku yake ba ku, za su kuma shari'anta mutane ba nuna bambanci. 19 Kada ku
ɓata shari'a, ko ku nuna bambanci. Kada ku karɓi cin hanci, gama cin hanci yakan
makanta idanu mai hikima, yǎ murɗe maganar mai gaskiya. 20 Gaskiya ce kaɗai za
ku bi don ku rayu, ku kuma mallaki ƙasar da UBANGIJI Allahnku yake ba ku.

*Yin sujada wa waɗansu alloli*
21 Kada ku kafa wani ginshiƙin itacen Ashera* kusa da bagaden da kuka gina wa

* **16:21** Ko Kada ku shuka wani itacen da aka miƙa wa Ashera

Ubangiji Allahnku, 22 kada kuma ku tayar da dutse mai tsarki, gama waɗannan ne
Ubangiji Allahnku yana ƙi.

## 17

1 Kada ku miƙa wa Ubangiji Allahnku, saniya ko tunkiyar da take da wani lahani,
ko naƙasa a cikinta, gama wannan zai zama abar ƙyama gare shi.

2 In an sami wani namiji ko ta mace mai zama a cikinku, a ɗaya daga biranen da
Ubangiji ya ba ku yana aikata abin da yake mugu a gaban Ubangiji Allahnku ta wurin
karya alkawarinsa, 3 wanda ya saba wa umarnina, har ya yi sujada ga waɗansu alloli,
yana rusuna musu, ko ga rana, ko ga wata, ko kuwa ga taurarin sama, 4 in kuwa aka
faɗa muku wannan, to, dole a bincika sosai. In kuwa gaskiya ne, aka kuma tabbatar
cewa wannan abin ƙyama ya faru a cikin Isra’ila, 5 sai a ɗauki namijin, ko ta mace
wanda ya aikata wannan mugun abu zuwa ƙofar birni, a jajjefe wannan mutum sai
ya mutu. 6 Bisa ga shaidar mutum biyu ko uku, za a iya kashe mutum, amma ba za
a iya kashe mutum bisa ga shaida mutum guda ba. 7 Hannuwan shaidun ne za su
zama na farko a kisan wanda ake zargin, sa’an nan hannuwan dukan mutane. Dole
ku fid da mugu daga cikinku.

### *Kotunan Shari’a*

8 In aka kawo ƙarar da yake da wuya sosai ga alƙali a kotunanku, ko wadda aka
zub da jini ne, ko ta faɗa ce, ko kuwa ta wadda aka ci mutunci ce, ku kai su wurin
da Ubangiji Allahnku zai zaɓa. 9 Ku je wurin firistoci, waɗanda suke Lawiyawa, ga
kuma alƙalin wanda yake mulki a lokacin. Ku bincika daga gare su, za su kuwa ba da
hukunci. 10 Dole ku aikata hukuncin da suka yi a wurin da Ubangiji zai zaɓa. Ku lura
fa, ku aikata kome da suka faɗa muku. 11 Ku yi bisa ga dokar da suka koyar muku
da kuma hukuncin da suka yi muku. Kada ku juya daga abin da suka faɗa muku, ko
zuwa dama, ko zuwa hagu. 12 Duk mutumin da ya yi rashin hankali wa alƙali, ko ga
firist wanda yake aiki a nan wa Ubangiji Allahnku, dole a kashe shi. Dole ku fid da
mugu daga Isra’ila. 13 Dukan mutane kuwa za su ji, su kuma ji tsoro, ba kuwa za su
ƙara yin rashin hankali kuma ba.

### *Sarki*

14 Sa’ad da kuka shiga ƙasar da Ubangiji Allahnku yake ba ku, kuka mallake ta,
kuka kuma zauna a cikinta, sai kuka ce, “Bari mu naɗa sarki a kanmu kamar sauran
al’umman da suke kewaye da mu,” 15 ku tabbata kun naɗa sarki a kanku wanda
Ubangiji Allahnku ya zaɓa ne. Dole yă zama daga cikin ’yan’uwanku. Kada ku sa
baƙo a kanku, wanda ba mutumin Isra’ila ɗan’uwanku ba. 16 Sarkin, ba zai nemi
dawakai da yawa wa kansa ba, ko yă sa mutane su koma Masar don su sami ƙarin
dawakai ba, gama Ubangiji ya faɗa muku, “Ba za ku ƙara koma wancan hanya kuma
ba.” 17 Sarkin ba zai auri mata masu yawa ba, in ba haka ba zuciyarsa za tă karkata.
Ba zai tara azurfa da zinariya da yawa ba.

18 Sa’ad da ya hau kursiyin mulkinsa, sai yă rubuta wa kansa a littafin kofin wannan
doka da aka ɗauka daga na firistoci, waɗanda suke Lawiyawa. 19 Zai kasance tare da
shi, zai kuma karanta shi dukan kwanakin ransa, saboda yă koyi girmama Ubangiji
Allahnsa, yă kuma bi dukan kalmomin wannan doka da kuma waɗannan ƙa’idodi
a hankali 20 don kada yă ɗauki kansa ya fi ’yan’uwansa, yă kuma juya daga dokar
zuwa dama, ko zuwa hagu. Sa’an nan shi da kuma zuriyarsa za su daɗe suna mulki
a Isra’ila.

# 18

*Hadayu saboda Firistoci da Lawiyawa*
*(Kidaya 18.8-32)*

1 Firistocin da suke Lawiyawa, tabbatacce dukan kabilar Lawi, ba za su sami rabo
ko gādo tare da Isra’ila ba. Za su yi rayuwa a kan hadayun da aka kawo wa Ubangiji
da wuta ne, gama wannan ne gādonsu. 2 Ba za su sami gādo a cikin ’yan’uwansu ba;
Ubangiji ne gādonsu, kamar yadda ya yi musu alkawari.
3 To, ga rabon da jama’a za su ba firistoci daga hadayun da suka miƙa ta bijimi ne,
ko ta tunkiya ce; sai su ba firistoci kafaɗar, kumatun, da kuma kayan cikin. 4 Za ku
ba su nunan fari na hatsinku, da sabon ruwan inabinku, da manku, da kuma gashi
na fari daga askin da kuka yi na tumakinku. 5 Gama Ubangiji Allahnku ya zaɓe su
da zuriyarsu daga cikin dukan kabilanku don su tsaya su yi hidima a cikin sunan
Ubangiji har abada.
6 Idan Balawe ya tashi daga wani garinku, wurin da yake da zama a Isra’ila, ya tafi
a wurin da Ubangiji ya zaɓa, zai iya dawo a duk lokacin da ya ga dama. 7 Zai iya yin
hidima a cikin sunan Ubangiji Allahnsa kamar dukan sauran ’yan’uwansa Lawiyawa
waɗanda suke hidima a can, a gaban Ubangiji. 8 Zai sami rabo daidai da sauran, ko
da yake ya karɓi kuɗin mallaka na iyali da ya sayar.

*Ayyukan Banƙyama*

9 Sa’ad da kuka shiga ƙasar da Ubangiji Allahnku yake ba ku, kada ku kwaikwayi
hanyoyin banƙyama na al’ummai da suke can. 10 Kada a sami wani a cikinku
da ya miƙa ɗansa, ko ’yarsa a wuta, ko a sami mai duba, ko mai maita, ko mai
fassara gaibi, ko mai sihiri, 11 ko boka, ko mabiya, ko maye, ko mai sha’ani da
matattu. 12 Duk wanda yake yin waɗannan abubuwa, shi abin ƙyama ne ga Ubangiji,
saboda waɗannan abubuwa banƙyama ne kuwa Ubangiji Allahnku ya kori waɗancan
al’ummai kafin ku. 13 Dole ku zama marasa zargi a gaban Ubangiji Allahnku.

*Annabi*

14 Al’ummai da za ku kora sukan saurari waɗannan masu maita, ko masu duba.
Amma ku, Ubangiji Allahnku bai yarda muku ku yi haka ba. 15 Ubangiji Allahnku zai
tayar muku da wani annabi kamar ni daga cikin ’yan’uwanku. Dole ku saurare shi.
16 Gama abin da kuka nema daga Ubangiji Allahnku ke nan a Horeb, a ranar taro,
sa’ad da kuka ce, “Kada ka bari mu ji muryar Ubangiji Allahnmu, ko mu ƙara ganin
wuta mai girma, in ba haka ba, za mu mutu.”
17 Sai Ubangiji ya ce mini, “Abin da suka faɗa yana da kyau. 18 Zan tayar musu da
wani annabi kamar ka daga cikin ’yan’uwansu; zan sa kalmomina a cikin bakinsa,
zai kuma faɗa musu kome da na umarce shi. 19 Duk wanda bai saurari kalmomina
da annabin nan yake magana da sunana ba, ni kaina zan nemi hakki a kan mutumin.
20 Amma duk annabin da ya ɗauka cewa yana magana da sunana a kan wani abin
da ban umarce shi ya faɗa ba, ko kuwa wani annabin da ya yi magana da sunan
waɗansu alloli, dole a kashe shi.”
21 Mai yiwuwa ku ce wa kanku, “Yaya za mu san cewa wannan saƙo ba Ubangiji
ne ya faɗa ba?” 22 In abin da annabin ya furta da sunan Ubangiji bai faru ba, ko
bai zama gaskiya ba, saƙo ne da Ubangiji bai faɗa ba ke nan. Wannan annabi ya yi
rashin hankali ne kawai. Kada ku ji tsoronsa.

# 19

*Biranen Mafaka*
*(Kidaya 35.9-28; Yoshuwa 20.1-9)*

1 Sa'ad da UBANGIJI Allahnku ya hallakar da al'ummai waɗanda yake ba ku ƙasarsu,
sa'ad da kuka kore su, kuka kuma zauna a birane da gidajensu, 2 sai ku keɓe wa
kanku birane uku waɗanda suke a tsakiyar ƙasar da UBANGIJI Allahnku yake ba
ku ku mallaka. 3 Ku gina hanyoyi zuwa cikinsu, ku kuma raba ƙasar da UBANGIJI
Allahnku yake ba ku gādo kashi uku, saboda duk wani da ya yi kisankai yǎ iya gudu
zuwa can.
4 Ga doka game da mutumin da ya kashe wani, ya kuma gudu don yǎ cece ransa,
wani wanda ya kashe maƙwabcinsa ba da gangan ba, ba kuwa da wata ƙiyayya a
tsakaninsu a dā ba. 5 Misali, in mutum ya je jeji da maƙwabcinsa domin yankan
itace, sai ruwan gatarinsa ya kwaɓe daga ƙotar yayinda yake saran itacen, ya sari
maƙwabcin har ya mutu. Mutumin nan zai iya gudu zuwa ɗaya daga cikin waɗannan
birane don yǎ ceci ransa. 6 In ba haka ba mai neman ɗaukan fansa jini, zai iya binsa
cikin fushi, yǎ cim masa, saboda nisan hanyar, har ya kashe shi, ko da yake bai
cancanci mutuwa ba, tun da yake ba ƙiyayya tsakaninsa da abokinsa a dā. 7 Wannan
ne ya sa na umarce ku ku keɓe wa kanku birane uku.
8 In UBANGIJI Allahnku ya fadada yankinku, kamar yadda ya alkawarta da rantsuwa
wa kakanninku, ya kuma ba ku ƙasar gaba ɗaya kamar yadda ya yi musu alkawari,
9 idan dai kun lura, kuka kiyaye umarnin da nake ba ku a yau, wato, ta wurin ƙaunar
UBANGIJI Allahnku, kuka kuma yi tafiya kullum cikin hanyoyinsa, to, sai ku keɓe ƙarin
birane uku. 10 Ku yi haka don kada a zub da jinin marar laifi a ƙasar da UBANGIJI
Allahnku yake ba ku gādo, don kada ku kuma zama masu laifin zub da jini.
11 Amma idan wani mutum yana ƙin maƙwabcinsa, ya kuma yi kwanto yana
fakonsa, ya yi masa rauni, har ya kashe shi, sa'an nan ya gudu zuwa ɗaya daga
cikin waɗannan birane, 12 dattawan garinsa za su aika a kawo shi, a dawo da shi
daga birnin, a miƙa shi ga mai neman fansar jini don yǎ kashe shi. 13 Kada ku ji
tausayinsa. Dole ku fid da laifin zub da jinin marar laifi daga Isra'ila, don ku sami
zaman lafiya.
14 Kada ka gusar da dutsen nuna shaidar iyakar maƙwabcinka wanda kakanni suka
sa, a gādon da ka samu a ƙasar da UBANGIJI Allahnka yake ba ka mallaka.

### *Shaidu*

15 Shaidar mutum guda ba tǎ isa a tabbatar cewa mutum yana da laifi game da
laifin da ake tuhumarsa ba, ko kuwa a kan wani laifin da ake zaginsa da aikata ba.
Dole a tabbata da batun ta bakin shaidu biyu, ko uku.
16 In wani ɗan sharri ya tashi ya yi wa wani sharri, don a sami wani da laifi, 17 dole
mutanen nan biyu da suke rikici su tsaya a gaban UBANGIJI, a gaban firistoci da alƙalai
waɗanda suke aiki a lokacin. 18 Dole alƙalan su yi bincike sosai, in kuma aka tabbatar
mai ba da shaida maƙaryaci ne, yana ba da shaidar zur a kan ɗan'uwansa ne, 19 to,
sai a yi da shi yadda ya yi niyya yǎ yi da ɗan'uwansa. Dole ku fid da mugu daga
cikinku. 20 Sauran mutane za su ji wannan su kuma ji tsoro, ba kuwa za a ƙara yin
irin wannan mugun abu a cikinku ba. 21 Kada ku ji tausayi, rai yǎ zama a maimakon
rai, ido a maimakon ido, haƙori a maimakon haƙori, hannu a maimakon hannu, ƙafa
a maimakon ƙafa.

## 20

### *Tafiya yaƙi*

1 Sa'ad da kuka tafi yaƙi da abokan gābanku, kuka ga dawakai da kekunan yaƙi da
kuma mayaƙan da suka fi ku yawa, kada ku ji tsoronsu, domin UBANGIJI Allahnku,
wanda ya fitar da ku daga Masar zai kasance tare da ku. 2 Sa'ad da kuke gab da kama
yaƙi, sai firist yǎ zo gaba yǎ yi wa mayaƙan jawabi. 3 Zai ce, "Ku ji, ya Isra'ila, yau
kuna gab da kama da abokan gābanku. Kada ku karai, ko ku ji tsoro; kada ku firgita,

ko ku yi rawar jiki a gabansu. 4 Gama UBANGIJI Allahnku, yana tafe tare da ku, zai
yaƙi abokan gābanku dominku, yă ba ku nasara."
5 Hafsoshi za su ce wa mayaƙa, "Ko akwai wanda ya gina sabon gida bai kuma
buɗe shi ba? Bari yă tafi gida, kada yă mutu a yaƙi, wani dabam yă buɗe shi. 6 Ko
akwai wani da ya shuka inabi, bai kuwa fara jin daɗinsa ba? Bari yă tafi gida, kada
yă mutu a yaƙi, wani dabam yă ji daɗinsa. 7 Ko akwai wani da aka yi masa alkawarin
mata, bai kuwa aure ta ko ba? Bari yă tafi gida, kada yă mutu a yaƙi, wani dabam yă
aure ta." 8 Sa'an nan hafsoshin za su ƙara da cewa, "Ko akwai wani da yake tsoro,
ko ya karai? Bari yă tafi gida don kada 'yan'uwansa su karai su ma." 9 Sa'ad da
hafsoshin suka gama magana da mayaƙan, sai su naɗa komandodi a kansu.
10 Sa'ad da kuka haura don ku fāɗa wa birni, sai ku fara neman garin da salama.
11 In sun yarda da salamar, suka buɗe ƙofofin garinsu, to, sai dukan mutanen da suke
cikinsa su yi muku aikin gandu, su kuma yi muku aiki. 12 In kuwa suka ƙi salamar,
suka fāɗa muku da yaƙi, sai ku yi wa wannan birni ƙawanya. 13 Sa'ad da UBANGIJI
Allahnku ya ba da shi cikin hannunku, sai ku kashe dukan mazan da suke cikinsa
da takobi. 14 Game da mata, yara, dabbobi da kuma sauran abubuwan da suke cikin
birnin, za ku iya kwasa waɗannan a matsayin ganima wa kanku. Za ku kuma yi
amfani da ganimar da UBANGIJI Allahnku ya ba ku daga abokan gābanku. 15 Haka za
ku yi da dukan biranen da suke nesa da ku, waɗanda kuma ba na al'ummai da suke
kusa ba.
16 Amma fa, a cikin biranen al'ummai da UBANGIJI Allahnku yake ba ku gādo, kada
ku bar wani abu mai numfashi da rai. 17 Ku hallaka su ƙaƙaf, wato, Hittiyawa,
Amoriyawa, Kan'aniyawa, Ferizziyawa, Hiwiyawa da kuma Yebusiyawa, yadda
UBANGIJI Allahnku ya umarce ku. 18 In ba haka ba, za su koya muku ku bi dukan
abubuwan banƙyaman da suke yi, ta yin sujada wa allolinsu, ta haka kuwa ku yi wa
UBANGIJI Allahnku zunubi.
19 Sa'ad da kuka yi wa birni ƙawanya kuka daɗe, kuka yi ta yaƙi don ku ci shi, kada
ku sassare itatuwansa da gatari, domin za ku ci 'ya'yansu. Kada ku sassare su. Gama
itatuwan da suke cikin gonaki, ba mutane ne da za ku yi musu ƙawanya? 20 Amma
fa, za ku iya sassare itatuwan da kuka sani ba sa ba da 'ya'ya, ku kuma yi amfani da
su don ayyukan gina ƙawanyar, sai an ci birnin da yaƙi.

# 21

*Kafara don kisankan da ba a warware ba*

1 In aka sami an kashe mutum kwance a fili, a ƙasar da UBANGIJI Allahnku yake ba
ku ku mallaka, ba a kuma san wanda ya kashe shi ba, 2 sai dattawanku da alƙalanku
su je su gwada nisan wurin da gawar take zuwa garuruwan da suke maƙwabtaka.
3 Sai dattawan garin da suke kurkusa da gawar su ɗauki karsanar da ba a taɓa yin aiki
da ita ba, ba a kuma taɓa sa mata karkiya ba, 4 a gangara da ita kwarin da ba a taɓa
nome, ko shuki a ciki ba, inda kuma akwai rafi mai gudu, a can cikin kwarin za su
karye wuyanta. 5 Firistoci, 'ya'yan Lawi maza, za su fito, gama UBANGIJI Allahnku ya
zaɓe su su yi masa hidima, su kuma furta albarku a cikin sunan UBANGIJI, za su kuma
daidaita duk rigimar cin mutunci. 6 Sa'an nan dukan dattawan garin da yake kurkusa
da gawar za su wanke hannuwansu a bisa karsanan da aka karye wuyar a kwarin,
7 za su kuma furta, "Hannuwanmu ba su zub da wannan jini ba, idanunmu kuma
ba su ga an yi haka ba. 8 Karɓi wannan kafara saboda mutanenka Isra'ila, wanda ka
fansar, ya UBANGIJI, kada kuma ka ɗaura wa mutanenka alhakin jinin mutumin nan
marar laifi." Za a kuwa yi kafarar zub da jinin da aka yi. 9 Ta haka za ku fid da laifin
zub da jinin marar laifi daga cikinku, da yake kun yi abin da yake daidai a gaban
UBANGIJI.

*Auren matan da aka kama daga yaƙi*

10 Sa'ad da kuka tafi yaƙi da abokan gābanku, sai UBANGIJI Allahnku ya bashe su a
hannuwanku kuka kuma kama su a matsayin bayi, 11 in ka ga wata kyakkyawar mace
wadda ta ɗauki hankalinka a cikin bayin, za ka iya aure ta tă zama matarka. 12 Ka
kawo ta gidanka ka sa tă aske kanta, tă yanka kumbanta 13 tă kuma tuɓe tufafin da ta
sa sa'ad da aka kama ta. Bayan ta zauna a gidanka ta kuma yi makokin mahaifinta da
mahaifiyarta wata ɗaya cif, sai ka shiga wurinta ka zama mijinta, za tă kuwa zama
matarka. 14 In ba ka jin daɗinta, ka bar tă tafi inda take so. Ba za ka sayar da ita ko
ka yi da ita kamar baiwa ba, da yake ka ƙasƙantar da ita.

*'Yancin ɗan fari*

15 In mutum yana da mata biyu, yana kuwa ƙaunar ɗaya, ba ya kuma ƙaunar
ɗayan, su biyun kuwa suka haifi masa 'ya'ya maza, sai ya zamana cewa ɗan farin ya
kasance na wadda ba ya ƙauna, 16 to, a ranar da zai yi faɗa wane ne a cikin 'ya'yansa
zai riƙe gādon da zai bar musu, kada yă sa ɗan matar da yake ƙauna yă zama kamar
shi ne ɗan fari, a maimakon ɗan matar da ba ya ƙauna, wanda shi ne ɗan farin.
17 Dole yă yarda cewa ɗan matar da ba ya ƙaunar ne ɗan fari, ta wurin ba shi rabo
kashi biyu na dukan abin da yake da shi, gama shi ne mafarin ƙarfinsa, yana da
hakkin ɗan fari.

*Gagararren ɗa*

18 In mutum yana da gagararren ɗa mai tawaye, wanda ba ya biyayya ga mahaifinsa
da mahaifiyarsa, ba ya kuma jin su sa'ad da suke horonsa, 19 mahaifinsa da
mahaifiyarsa za su kama shi su kawo shi ga dattawa a ƙofar garinsu. 20 Za su ce
wa dattawan, "Wannan ɗanmu gagararre ne, mai tawaye. Ba ya mana biyayya. Mai
zari ne, kuma mashayi." 21 Sa'an nan dukan mazan garinsa za su jajjefe shi har yă
mutu. Dole ku fid da mugu daga cikinku. Dukan Isra'ila kuwa za su ji wannan su
kuma ji tsoro.

*Waɗansu dokoki*

22 In mutum ya yi laifin da ya isa kisa, aka kuwa rataye shi a itace, 23 kada ku bar
jikinsa a kan itacen yă kwana. Ku tabbata kun binne shi a ranar, domin duk wanda
aka rataye a kan itace la'ananne ne ga Allah. Kada ku ƙazantar da ƙasar da UBANGIJI
Allahnku yake ba ku gādo.

# 22

1 In kun ga saniya ko tunkiyar ɗan'uwanku wadda ta ɓace, kada ku ƙyale ta, amma
ku tabbata kun komar da ita gare shi. 2 In ɗan'uwan ba ya zama kusa da ku, ko kuwa
ba ku san shi ba, sai ku kai ta gida ku ajiye ta sai ya zo nemanta. Sa'an nan ku ba
shi ita. 3 Ku yi haka in kun sami jakin ɗan'uwanku, ko rigarsa, ko kowane abin da
ya ɓace. Kada ku ƙyale shi.

4 In kuka ga jakin ɗan'uwanku, ko saniyarsa ya fāɗi a kan hanya, kada ku ƙyale
shi. Ku taimaka, ku tā da shi.

5 Kada mace ta sa suturar maza, kada kuma namiji ya sa suturar mata, gama
UBANGIJI Allahnku yana ƙyamar duk mai yin haka.

6 In kuka ga gidan tsuntsu kusa da hanya, ko a kan itace, ko kuma a ƙasa,
mahaifiyar tsuntsun kuwa tana kwance a kan 'ya'yanta, ko kuwa a kan ƙwanta,
kada ku kama mahaifiyar duk da 'ya'yan. 7 Za ku iya kwashe 'ya'yan, amma ku
tabbata kun bar mahaifiyar tă tafi. Yin haka zai sa ku sami zaman lafiya da tsawon
rai.

8 Sa'ad da kuka gina sabon gida, ku ja masa dakali kewaye da rufinku don kada ku
jawo laifin zub da jini a kan gidanku in wani ya fāɗi daga kan rufin.

9 Kada ku shuka iri biyu a gonar inabinku; in kuka yi haka, ba abin da kuka shuka ne kaɗai zai ƙazantu ba, amma har da inabinku ma.
10 Kada ku haɗa bijimi da jaki su yi noma tare.
11 Kada ku sa rigar ulu da aka gauraye da lilin aka saƙa.
12 Ku yi tuntu a kusurwan huɗu na rigar da kuke sa.

*Dokoki game da hana lalata*

13 In mutum ya auri mace, bayan ya kwana da ita, sa'an nan ya ƙi ta 14 ya kuma
zarge ta, ya ba ta mummunan suna, yana cewa, "Na auri wannan mata, amma sa'ad
da na kusace ta, ban sami tabbaci cewa ita budurwa ba ce," 15 sai mahaifin yarinyar
da mahaifiyarta su kawo shaida cewa ita budurwa ce wa dattawan gari a ƙofar garin.
16 Mahaifin yarinyar zai ce wa dattawa, "Na ba da 'yata aure ga wannan mutum,
amma ya ƙi ta. 17 Yanzu ya zage ta cewa, 'Ban sami 'yarku budurwa ba.' Amma ga
shaidar budurcin 'yata." Sa'an nan iyayenta za su shimfiɗa zanen a gaban dattawan
garin, 18 dattawan kuwa za su ɗauki mutumin su hukunta shi. 19 Za su ci masa
tara shekel azurfa ɗari, su ba mahaifin yarinyar, domin wannan mutum ya ba wa budurwa mutuniyar Isra'ila mummunan suna. Za tă ci gaba da zama matarsa; ba kuwa zai sake ta ba muddin ransa.
20 Amma fa in zarge gaskiya ne, ba a kuwa sami shaidar budurcin yarinyar ba, 21 sai
a kawo ta a ƙofar gidan mahaifinta, a can mazan gari za su jajjefe ta da dutse har tă mutu. Ta yi abin kunya a Isra'ila ta wurin lalaci a yayinda take a gidan mahaifinta. Dole ku fid da mugu daga cikinku.
22 In aka kama wani yana kwance da matar wani, dole a kashe dukansu biyu, wato, mutumin da ya kwana da matar da kuma matar. Dole a fid da mugu daga Isra'ila.
23 In mutum ya sadu da budurwa a gari wadda aka yi alkawarin aure, ya kuma
kwana da ita 24 sai ku ɗauki su biyu zuwa ƙofar wannan gari, ku jajjefe su da dutse har su mutum, za a kashe yarinyar domin tana a cikin gari ba ta kuwa yi ihu neman taimako ba, za a kashe mutumin domin ya yi lalata da matar wani. Dole ku fi da mugu daga cikinku.
25 Amma in a bayan gari ne mutumin ya sadu da yarinyar da aka yi alkawari aure,
ya kuma yi mata fyaɗe, mutumin da ya yi wannan ne kaɗai zai mutu. 26 Kada ku yi
wa yarinyar kome, ba tă yi zunubin da ya cancanci mutuwa ba. Wannan batu ya yi kamar da na mutumin da ya fāɗa wa maƙwabcinsa ya kuma kashe shi. 27 Tun da ya
same ta a jeji ne, wataƙila yarinyar ta yi kukan neman taimako, amma babu wani da zai cece ta.
28 In mutum ya sadu da yarinyar da ba a yi alkawarin aurenta ba, ya kuma yi mata
fyaɗe, aka kuma kama su, 29 sai yă biya mahaifin yarinyar shekel hamsin na azurfa.
Dole yă auri yarinyar, gama ya yi lalata da ita. Ba zai taɓa sake ta ba muddin ransa.
30 Kada mutum yă auri matar mahaifinsa, kada yă ƙasƙantar gādon mahaifinsa.

# 23

*Warewa daga taro*

1 Duk wanda aka daƙe, ko yanke gabansa, ba zai shiga taron jama'ar UBANGIJI ba.
2 Duk wanda aka haifa ta wurin cikin shege, har tsara ta goma, zuriyarsa ba za su shiga taron jama'ar UBANGIJI ba, har zuwa tsara ta goma.
3 Ba mutumin Ammon, ko mutumin Mowab, ko kuwa wani zuriyarsu da zai shiga
taron jama'ar UBANGIJI, har tsara ta goma. 4 Gama ba su zo sun tarye ku da burodi
da ruwa a hanyarku, sa'ad da kuka fito daga Masar ba, sai ma suka yi haya Bala'am ɗan Beyor daga Fetor a Aram-Naharayim* yă furta la'ana a kanku. 5 Amma UBANGIJI

* **23:4** Wato, Arewa maso yamma na Mesofotamiya

Allahnku bai saurari Bala'am ba, sai ya mai da la'anar ta koma albarka gare ku,
domin Ubangiji Allahnku yana ƙaunarku. 6 Kada ku yi yarjejjeniyar abuta da su,
muddin kuna da rai.
7 Kada ku yi ƙyamar mutumin Edom, gama mutumin Edom ɗan'uwanku ne. Kada
ku yi ƙyamar mutumin Masar, domin kun yi zama baƙunta a ƙasarsa. 8 'Ya'yan da
aka haifa musu na tsara ta uku za su iya shiga taron jama'ar Ubangiji.

### *Kiyaye sansanin yaƙi da tsabta*

9 Sa'ad da kuka yi sansani don ku yi yaƙi da abokan gābanku, ku kiyaye kanku daga
duk wani abu marar tsabta. 10 In ɗaya daga cikin mazanku ya ƙazantu saboda zubar
da maniyyi, sai yă fita daga sansani yă zauna waje da sansani. 11 Amma yayinda
yamma ke gabatowa sai yă wanke kansa, da fāɗuwar rana kuwa sai yă koma cikin
sansani.
12 Ku keɓe wuri waje da sansani inda za ku iya zuwa don yin bayan gari. 13 Sai ku
ɗauki wani abin tona ƙasa, sa'ad da kuka yi bayan gari, sai ku tona rami, ku rufe
bayan garinku. 14 Gama Ubangiji Allahnku yana zagawa a cikin sansaninku don yă
tsare ku, yă kuma bashe abokan gābanku gare ku. Dole sansaninku yă kasance da
tsarki, saboda kada yă ga wani abu marar kyau a cikinku, har yă juya daga gare ku.

### *Waɗansu dokoki*

15 In bawa ya tsere zuwa wurinku don mafaka, kada ku miƙa shi ga ubangidansa.
16 Ku bar shi yă zauna a cikinku a duk inda yake so, da kuma a kowane garin da ya
zaɓa. Kada ku tsananta masa.
17 Kada mutumin Isra'ila ko mutuniyar Isra'ila yă zama karuwar haikali. 18 Kada
ku kawo kuɗin a cikin gida Ubangiji Allahnku da aka samu ta wurin karuwanci
wanda mace ko namiji ya yi don biyan wani alkawari, domin Ubangiji Allahnku
yana ƙyamar su duka.
19 Kada ku nemi ɗan'uwanku yă biya bashin da kuka ba shi da ruwa, ko kuɗi,
ko abinci, ko kowane irin abin da yana iya ba da ruwa. 20 Za ku iya nemi ruwa a
bashin da kuka ba baƙo, amma ba ɗan'uwanku mutumin Isra'ila ba, domin Ubangiji
Allahnku yă sa muku albarka a kowane abin da kuka sa hannunku a kai, a ƙasar da
kuke shiga ku ci gādonta.
21 In fa kuka yi alkawari ga Ubangiji Allahnku, to, kada ku yi jinkirin cikawa, gama
tabbatacce Ubangiji Allahnku zai neme shi daga gare ku, za ku kuma zama masu
laifin zunubi. 22 Amma in ba ku yi alkawari ba, ba kuwa zai zama muku zunubi ba.
23 Duk abin da ya fita daga bakinku, sai ku lura ku cika shi, kamar yadda kuka yarda
da kanku, kuka yi alkawarin ga Ubangiji Allahnku da bakinku.
24 In kun shiga gonar inabin maƙwabcinku, za ku iya cin inabin da kuke so, amma
kada ku sa wani a kwandonku. 25 In kun shiga gonar hatsin maƙwabcinku, za ku iya
murmure tsabar da hannuwanku, amma kada ku sa lauje ku yanka hatsinsa da yake
tsaye.

## 24

1 Idan mutum ya auri mata, daga baya ba tă gamshe shi ba domin ya gano wani
abu marar kyau game da ita, ya ba ta takardar saki, ya kuma kore ta daga gidansa,
2 in bayan ta bar gidansa ta zama matar wani dabam, 3 sai mijinta na biyu ya ƙi ta, ya
ba ta takardan saki, ya kore ta daga gidansa, ko kuwa ya mutu, 4 to, kada mijinta na
farko, wanda ya sake ta yă sāke aurenta, tun da yake ta ƙazantu. Wannan zai zama
abin ƙyama a gaban Ubangiji. Kada ku kawo zunubi a ƙasar da Ubangiji Allahnku
yake ba ku gādo.
5 In mutum bai daɗe da aure ba, kada a sa yă je yaƙi, ko yă yi wani aiki. Gama zai
huta shekara guda a gida, yă faranta wa matar da ya aura rai.

6 Kada ku karɓi jinginar dutsen niƙa tare da ɗan dutsen niƙan, domin yin haka zai
zama karɓar jinginar rai ne.
7 Idan aka kama wani yana satar ɗan’uwansa mutumin Isra’ila domin yǎ sa ya
zama bawansa, ko yǎ sayar da shi, sai a kashe ɓarawon nan. Haka za ku kawar da
mugunta daga cikinku.
8 Game da cututtukan kuturta, sai ku lura, ku yi yadda firistocin da suke Lawiyawa
suka umarce ku. Dole ku lura ku bi abin da na umarce su. 9 Ku tuna da abin da
UBANGIJI Allahnku ya yi wa Miriyam a hanya, bayan kun fito Masar.
10 Sa’ad da kuka ba da rance na kowane iri ga maƙwabcinku, kada ku shiga gidansa
don karɓar wani abu a matsayin jingina. 11 Ku tsaya a waje ku bar mutumin da yake
karɓan rancen yǎ kawo muku abin da zai bayar a matsayin jingina. 12 In matalauci
ne, kada ku kwana da abin da zai bayar a matsayin jingina a wurinku. 13 Ku mayar
da rigarsa a fāɗuwar rana saboda yǎ sami abin rufuwa. Yin haka zai sa yǎ gode
muku, za a kuma ɗauka wannan a matsayin aikin adalci da kuka yi a gaban UBANGIJI
Allahnku.
14 Kada ku zalunci ɗan ƙodago matalauci da mabukaci, ko da shi ɗan’uwanku ne
mutumin Isra’ila, ko baƙon da yake zama a cikin garuruwanku. 15 Ku biya kuɗin
aikinsa kowace rana kafin fāɗuwar rana, domin shi matalauci ne, yana kuma sa rai
a kan wannan hakkin ne, don kada ya yi wa UBANGIJI kuka a kanku, har yǎ zama
laifi a gare ku.
16 Ba za a kashe iyaye a maimakon ’ya’yansu ba, ba kuwa za a kashe ’ya’ya a
maimakon iyayensu ba; kowa ya yi zunubi, shi za a kashe.
17 Ba za ku danne hakkin baƙon da yake zama a cikinku ko na marayu ba, ba za ku
ɗauki rigar matar da mijinta ya mutu a matsayin jingina ba. 18 Ku tuna dā ku bayi
ne a Masar, UBANGIJI Allahnku kuwa ya fisshe daga can. Shi ya sa na umarce ku ku
yi wannan.
19 Sa’ad da kuke girbi a gonarku, sai kuka manta da dami, kada ku koma don ku
ɗauka. Ku bar shi don baƙo, maraya da kuma gwauruwa, saboda UBANGIJI Allahnku
yǎ albarkace ku a cikin dukan aikin hannuwanku. 20 Sa’ad da kuka kakkaɓe ’ya’yan
zaitun daga itatuwanku, kada ku yi kalan abin da ya rage. Ku bar shi don baƙo,
maraya da kuma gwauruwa. 21 Sa’ad da kuka yi girbin inabi a gonar inabinku, kada
ku yi kalan abin da ya rage. Ku bar shi don baƙo, maraya da kuma gwauruwa. 22 Ku
tuna dā ku bayi ne Masar. Shi ya sa na umarce ku ku yi wannan.

# 25

1 Idan mūsu ya tashi tsakanin mutum biyu har abin ya kai su kotu, alƙalai kuwa
suka yanke hukunci a kan batun, suka kuɓutar da marar laifi sa’an nan suka hukunta
mai laifi, 2 in mai laifin ya cancanci bulala, alƙali zai sa yǎ kwanta a yi masa bulala a
gabansa da yawan bulalan da ya dace da laifin, 3 amma kada yǎ yi masa bulala fiye
da arba’in. In ya yi masa fiye da haka, za a ƙasƙantar da ɗan’uwanku, zai kuma
zama rainanne a idonku.
4 Kada ku yi wa saniya takunkumi sa’ad da take tattaka hatsi.
5 In ’yan’uwa suna zama tare, in ɗayansu ya mutu babu ɗa, kada gwauruwar tǎ yi
aure waje da iyalin. Ɗan’uwan mijinta zai ɗauke ta, yǎ aure ta, yǎ kuma cika abin
da yǎ kamaci ɗan’uwan miji yǎ yi. 6 Ɗan farin da ta haifa zai ɗauki sunan ɗan’uwan
da ya rasu saboda kada sunansa yǎ ɓace daga Isra’ila.
7 Amma fa, in mutum ba ya so yǎ auri matar ɗan’uwansa, sai tǎ tafi wurin dattawa
a ƙofar gari tǎ ce, “Ɗan’uwan mijina ya ƙi yǎ wanzar da sunan ɗan’uwansa a Isra’ila.
Ya ƙi yǎ cika abin da ya kamaci ɗan’uwan miji yǎ yi gare ni.” 8 Sai dattawan garinsa
su kira shi, su kuma yi masa magana. In ya nace yana cewa, “Ba na so in aure ta,”

9 sai gwauruwan nan, matar ɗan'uwansa tă haura wurinsa a gaban dattawa, tă tuɓe
takalminsa guda, ta tofa masa miyau a fuska, tă ce, "Haka za a yi ga mutumin da zai
ƙi kafa gidan ɗan'uwansa." 10 Za a kira zuriyarsa a Isra'ila Iyalin da aka tuɓe masa
takalmi.

11 In mutane biyu suna faɗa, sai matar mutum ɗaya daga cikinsu ta zo don tă
kuɓutar da mijinta daga abokin faɗarsa, ta kuma miƙa hannu ta kama marainan
wancan, 12 sai ku yanke hannunta. Kada ku ji tausayinta.

13 Kada ku kasance da ma'auni iri biyu a jakarku, ɗaya babba, ɗaya ƙarami. 14 Kada
ku kasance da mudu iri biyu a jakarku, ɗaya babba, ɗaya ƙarami. 15 Dole ku kasance
da ma'aunin da kuma mudun da yake daidai, kuma na gaskiya, saboda ku yi tsawon
rai a ƙasar da Ubangiji Allahnku yake ba ku. 16 Gama Ubangiji Allahnku yana ƙyamar
duk mai yi waɗannan abubuwa, da kuma mai rashin gaskiya.

17 Ku tuna da abin da Amalekawa suka yi muku a hanya, sa'ad da kuka fito Masar.
18 Yadda suka yi muku kwanto a hanya, suka fāɗa muku ta baya, suka karkashe
waɗanda suka gaji tiɓis. Ba su ko ji tsoron Allah ba. 19 Sa'ad da Ubangiji Allahnku
ya ba ku hutu daga dukan abokan gābanku kewaye da ku, a ƙasar da yake ba ku
ku mallaka a matsayin gādo, sai ku shafe Amalekawa daga duniya, don kada a ƙara
tunawa da su. Kada fa ku manta!

# 26

*'Ya'yan fari da kuma zakka*

1 Sa'ad da kuka shiga ƙasar da Ubangiji Allahnku yake ba ku gādo, kuka mallake
ta, kuka kuma zauna a cikinta, 2 sai ku ɗauki 'ya'yan fari na dukan amfanin gonar
ƙasar da Ubangiji Allahnku yake ba ku, ku zuba a kwando. Sa'an nan ku je wurin
da Ubangiji Allahnku ya zaɓa yă zama mazauni don Sunansa, 3 ku faɗa wa firist
da yake aiki a lokacin, "Na sakankance yau ga Ubangiji Allahnka, cewa na zo ƙasar
da Ubangiji ya rantse zai ba wa kakanninmu." 4 Firist ɗin zai karɓi kwandon daga
hannuwanku yă sa shi a ƙasa a gaban bagaden Ubangiji Allahnku. 5 Sa'an nan za
ku furta a gaban Ubangiji Allahnku cewa, "Mahaifina mutumin Aram ne mai yawo,
ya gangara zuwa Masar da mutane kaɗan, ya zauna a can, ya kuma zama babban
al'umma, mai iko da kuma mai yawa. 6 Amma Masarawa suka wulaƙanta mu suka
sa muka sha wahala, suna sa mu aikin dole. 7 Sai muka yi kuka ga Ubangiji Allahn
kakanninmu, Ubangiji kuwa ya ji kukanmu, ya kuma azabar da muke sha, da wahalar
da muke sha, da danniyar da suke yin mana. 8 Sai Ubangiji ya fitar da mu daga Masar
da hannu mai ƙarfi da kuma iko, da razana mai girma da kuma alamu banmamaki
da al'ajabai. 9 Ya kawo mu wannan wuri, ya kuma ba mu wannan ƙasa, ƙasa mai
zub da madara da kuma zuma; 10 yanzu kuwa na kawo 'ya'yan fari na gonar da kai,
ya Ubangiji ka ba ni." Sai ku sa kwandon a gaban Ubangiji Allahnku, sa'an nan ku
rusuna a gabansa. 11 Ku da Lawiyawa da baƙin da suke a cikinku, za ku yi murna
cikin dukan abubuwa masu kyau da Ubangiji Allahnku ya ba ku tare da gidanku.

12 Sa'ad da kuka gama fitar da kashi ɗaya bisa goma na dukan amfanin gona a
shekara ta uku, shekarar zakka, za ku ba da su ga Balawe, baƙo, maraya da kuma
gwauruwa, don su ci a cikin garuruwanku su ƙoshi. 13 Sa'an nan ku faɗa wa Ubangiji
Allahnku, "Na cire tsattsarkan rabo daga gidana na kuma ba wa Balawe, baƙo,
maraya da gwauruwa, bisa ga dukan abin da ka umarta. Ban ja gefe daga umarnanka
ko in manta da wani a cikinsu ba. 14 Ban ci wani daga cikin tsattsarkan rabo yayinda
nake makoki, ko in cire wani rabo mai tsarki yayinda nake marar tsarki, ko in miƙa
wani sashensa ga matattu ba. Na yi biyayya ga Ubangiji Allahna, na aikata kome
da ka umarce ni. 15 Ka duba ƙasa daga sama, mazauninka mai tsarki, ka albarkace

mutanenka Isra’ila da kuma ƙasar da ka ba mu kamar yadda ka yi wa kakanninmu
alkawari da rantsuwa, ƙasa mai zub da madara da zuma.”

*Ku bi umarnan UBANGIJI*

16 Yau UBANGIJI Allahnku ya umarce ku ku bi waɗannan ƙa’idodi da kuma dokoki,
cikin natsuwa ku kiyaye su da dukan zuciyarku da kuma dukan ranku. 17 Kun
furta a wannan rana cewa UBANGIJI shi ne Allahnku, cewa za ku kuma yi tafiya a
hanyoyinsa, cewa za ku kiyaye ƙa’idodinsa, umarnansa da kuma dokokinsa, kuka
kuma ce za ku yi masa biyayya. 18 UBANGIJI kuwa ya furta a wannan rana cewa ku
mutanensa ne, mallakarsa kamar yadda ya yi alkawari, da kuma cewa za ku kiyaye
dukan umarnansa. 19 Ya furta cewa zai sa ku zama masu yabo, masu suna, masu
daraja, fiye da dukan al’umman da ya yi. Za ku zama jama’a tsattsarka ta UBANGIJI
Allahnku, kamar yadda ya yi alkawari.

## 27

*Bagade a kan Dutsen Ebal*

1 Musa tare da dattawan Isra’ila suka umarci mutane suka ce, “Ku kiyaye dukan
umarnai da na ba ku a yau. 2 Sa’ad da kuka haye Urdun zuwa cikin ƙasar da UBANGIJI
Allahnku yake ba ku, ku kakkafa waɗansu manyan duwatsu, ku yi musu shafe da
farar ƙasa. 3 Ku rubuta dukan waɗannan kalmomin doka a kansu, sa’ad da kuka
haye kuka shiga ƙasar da UBANGIJI Allahnku yake ba ku, ƙasa mai zub da madara da
zuma, kamar dai yadda UBANGIJI Allah na kakanninku, ya yi muku alkawari. 4 Sa’ad
da kuma kuka haye Urdun, ku kakkafa waɗannan duwatsu a bisa Dutsen Ebal, kamar
yadda na umarce a yau, ku yi musu shafe da farar ƙasa. 5 Ku gina bagade wa UBANGIJI
Allahnku, bagaden dutse. Kada ku yi amfani da wani kayan aiki na ƙarfe a kansu.
6 Ku gina bagaden UBANGIJI Allahnku da duwatsun fili, ku kuma miƙa hadaya ta
ƙonawa a kansa ga UBANGIJI Allahnku. 7 Ku miƙa hadayun salama a can, kuna ci,
kuna farin ciki a gaban UBANGIJI Allahnku. 8 Za ku kuma rubuta a fayyace dukan
kalmomin wannan doka a kan waɗannan duwatsun da kuka kakkafa.”

*La’anu daga Dutsen Ebal*

9 Sai Musa da firistoci waɗanda suke Lawiyawa suka ce wa dukan Isra’ila, “Ku yi
shiru, ya Isra’ila, ku saurara! Yanzu kun zama mutanen UBANGIJI Allahnku. 10 Ku yi
biyayya ga UBANGIJI Allahnku, ku bi umarnansa da ƙa’idodin da nake ba ku a yau.”
11 A wannan rana Musa ya umarce mutane,

12 Sa’ad da kuka haye Urdun, sai waɗannan kabilai su tsaya a bisa Dutsen Gerizim
su sa wa jama’a albarka, wato, kabilar Simeyon, Lawi, Yahuda, Issakar, Yusuf da
Benyamin. 13 Waɗannan kabilai kuma za su tsaya a bisa Dutsen Ebal su furta la’ana,
wato, kabilar Ruben, Gad, Asher, Zebulun, Dan da Naftali.
14 Lawiyawa za su karanta wa dukan mutanen Isra’ila da babbar murya su ce,

15 “La’ananne ne mutumin da ya sassaƙa siffa, ko ya yi zubin gunki, abar ƙyama
ce ga UBANGIJI, aikin hannu mai sana’a da aka kafa a ɓoye.”
Sai dukan mutane su ce, “Amin!”
16 “La’ananne ne mutumin da ya ƙasƙantar da mahaifinsa ko mahaifiyarsa.”
Sai dukan mutane su ce, “Amin!”
17 “La’ananne ne mutumin da ya gusar da dutsen da aka kafa don nuna shaidar
iyaka.”
Sai dukan mutane su ce, “Amin!”
18 “La’ananne ne mutumin da ya karkatar da makaho daga hanya.”

Sai dukan mutane su ce, “Amin!”

19 “La’ananne ne mutumin da ya yi rashin adalci ga baƙo, maraya ko gwauruwa.”

Sai dukan mutane su ce, “Amin!”

20 “La’ananne ne mutumin da ya kwana da matar mahaifinsa, gama ya ƙasƙantar da gadon mahaifinsa ke nan.”

Sai dukan mutane su ce, “Amin!”

21 “La’ananne ne mutumin da ya yi jima’i da dabba.”

Sai dukan mutane su ce, “Amin!”

22 “La’ananne ne mutumin da ya kwana da ’yar’uwarsa, ’yar mahaifinsa ko ’yar mahaifiyarsa.”

Sai dukan mutane su ce, “Amin!”

23 “La’ananne ne mutumin da ya kwana da mahaifiyar matarsa.”

Sai dukan mutane su ce, “Amin!”

24 “La’ananne ne mutumin da ya kashe maƙwabcinsa a ɓoye.”

Sai dukan mutane su ce, “Amin!”

25 “La’ananne ne mutumin da ya karɓi cin hanci don yă kashe marar laifi.”

Sai dukan mutane su ce, “Amin!”

26 “La’ananne ne mutumin da bai yi na’am da kalmomin wannan doka ta wurin aikata su ba.”

Sai dukan mutane su ce, “Amin!”

# 28

### *Albarku don biyayya*

1 In kun yi biyayya da maganar Ubangiji Allahnku, kuka kuma lura, kuka bi dukan
umarnan da na ba ku a yau, Ubangiji Allahnku zai sa ku bisa dukan al’ummai a
duniya. 2 Dukan waɗannan albarku za su sauko muku, su zama naku, in kuka yi
biyayya ga Ubangiji Allahnku.

3 Za ku zama masu albarka a cikin birni, za ku kuma zama masu albarka har a ƙauye.

4 ’Ya’yanku za su zama masu albarka, haka ma hatsin gonakinku da kuma ’ya’yan dabbobinku, wato, ’ya’yan shanu da ’yan tumakinku.

5 Za a albarkaci kwandonku da kwanon kwaɓan kullunku.

6 Za ku zama masu albarka sa’ad da kuka shiga, za ku kuma zama masu albarka sa’ad da kuka fita.

7 A gabanku, Ubangiji zai sa ku fatattaki abokan gāban da za su taso suna gāba
da ku. Ta hanya guda za su auka muku, amma ta hanyoyi bakwai za su gudu daga
gabanku.

8 Ubangiji zai aika da albarka a rumbunanku da kuma a bisa kome da kuka sa hannunku a kai. Ubangiji Allahnku zai albarkace ku a ƙasar da yake ba ku.

9 Ubangiji zai kafa ku kamar mutanensa masu tsarki, kamar yadda ya yi alkawari
da rantsuwa, in kun kiyaye umarnan Ubangiji Allahnku, kuka kuma yi tafiya a
hanyoyinsa. 10 Sa’an nan dukan mutane a duniya za su ga cewa ana kiranku da
sunan Ubangiji, za su kuwa ji tsoronku. 11 Ubangiji zai azurta ku sosai, a ’ya’yan
cikinku, a ’ya’yan dabbobinku da kuma a hatsin gonarku, a cikin ƙasar da ya rantse
wa kakanninku zai ba ku.

12 Ubangiji zai buɗe sammai, wurin ajiyarsa mai yalwa, don yă aika da ruwan
sama a gonarku a lokacinsa, yă kuma albarkaci dukan aikin hannuwanku. Za ku ba
wa al’ummai masu yawa rance, amma ba za ku karɓa bashi daga wurin wani ba.
13 Ubangiji zai sa ku zama kai, ba wutsiya ba. In kun mai da hankali ga umarnan
Ubangiji Allahnku da nake ba ku a wannan rana, kuka kuma lura, kuka bi su, kullum

za ku kasance a bisa, ba a ƙasa ba. 14 Kada ku kauce zuwa dama ko zuwa hagu daga
umarnan da na ba ku a yau, har ku bi waɗansu alloli kuna yin musu sujada.

### *La'ana don rashi biyayya*
### *(Firistoci 26.14-46)*

15 Amma fa, in ba ku yi biyayya ga UBANGIJI Allahnku ba, ba ku kuma lura kun bi
dukan umarnansa da ƙa'idodin da nake ba ku a yau ba, dukan la'anan nan za su zo
a bisanku, su kuma same ku.
16 Za ku zama la'anannu a birni da kuma a ƙauye.
17 Za a la'anta kwandonku da kwanon kwaɓan kullunku.
18 Za a la'anta 'ya'yan cikinku, haka ma hatsin gonarku, da 'ya'yan shanunku da
'yan tumakinku.
19 Za a la'anta ku sa'ad da kuka shiga da sa'ad da kuka fita.
20 UBANGIJI zai aiko muku da la'ana, da ruɗewa, da damuwa cikin dukan abin da
za ku yi, har ya hallaka ku, ku lalace da sauri saboda mugayen ayyukanku, domin
kuma kuka rabu da ni.* 21 UBANGIJI zai aiko muku da annoba wadda za tă manne
muku, tă cinye ku cikin ƙasar da za ku shiga, ku mallake ta. 22 UBANGIJI zai buga ku
da cuta mai lalacewa, da zazzaɓi, da ƙuna, da zafin rana, da fāri, da burtuntuna, da
fumfuna, waɗanda za su azabtar da ku sai kun hallaka. 23 Girgijen da yake bisanku
zai zama tagulla, ƙasar da take ƙarƙashinku za tă zama ƙarfe. 24 UBANGIJI zai juye
ruwan saman ƙasarku yă zama ƙura da gari; zai sauko daga gizagizai har sai kun
hallaka.
25 UBANGIJI zai sa a rinjaye ku a gaban abokan gābanku. Ta hanya guda za ku auka
musu, amma ta hanyoyi bakwai za ku gudu daga gabansu. Za ku zama abin ƙi ga
dukan mulkokin duniya. 26 Gawawwakinku za su zama abincin dukan tsuntsayen
sarari da namun duniya, ba kuwa wanda zai kore su. 27 UBANGIJI zai buge ku da
maruran Masar, da ƙazuwa, da kuma ƙaiƙayi waɗanda ba za su warke ba 28 UBANGIJI
zai buge ku da hauka, makanta, da rikicewar hankali. 29 Da tsakar rana za ku riƙa
lallubawa kamar makaho. Za ku zama marasa nasara a cikin kome da kuka yi;
kowace rana za a zalunce ku, a kuma yi muku ƙwace, ba tare da wani ya cece ku ba.
30 Za ku yi tashin yarinya, amma wani ne zai ɗauke ta yă kwana da ita. Za ku gina
gida amma wani ne zai zauna a ciki. Za ku shuka inabi, amma ba za ku ma fara jin
daɗin 'ya'yansa ba. 31 Za a yanka sanku a idanunku, amma ba za ko ci wani abu a
cikinsa ba. Za a ƙwace jakinku ƙiri-ƙiri, amma ba za a mayar muku da shi ba. Za a
ba da tumakinku ga abokan gābanku, kuma ba kowa da zai cece su. 32 Za a ba da
'ya'yanku maza da mata ga wata al'umma, za ku kuma yi ta zuba idanunku kuna
neman su kullayaumi, amma a banza, domin ba ku da ikon yin kome. 33 Mutanen da
ba ku sani ba za su ci kayan gonarku da amfanin wahalarku, za a yi ta cucinku, ana
kuma danne ku kullum. 34 Abubuwan da za ku gani za su sa ku yi hauka. 35 UBANGIJI
zai buge gwiwoyinku da ƙafafunku da marurai masu zafi da ba za a iya warkar da
su ba, za su yaɗu daga tafin ƙafafu zuwa bisa kanku.
36 UBANGIJI zai kore ku, ku da sarkin da kuka naɗa a bisanku zuwa al'ummar da
ku, ko kakanninku ba su sani ba. A can za ku yi wa waɗansu alloli sujada, allolin
itace da na dutse. 37 Za ku zama abin ƙi, abin dariya, da kuma abin habaici ga dukan
al'ummai inda UBANGIJI zai kore ku zuwa.
38 Za ku shuka iri da yawa a gona, amma za ku girbe kaɗan, domin fāra za su
cinye su. 39 Za ku shuka inabi ku kuma yi musu banƙasa, amma ba za ku sha ruwan
inabin ba, domin tsutsotsi za su cinye su. 40 Za ku kasance da itatuwan zaitun ko'ina a
ƙasarku, amma ba za ku yi amfani da mansu ba, domin 'ya'yan zaitun za su kakkaɓe.

* **28:20** Da Ibraniyanci ni.

41 Za ku haifi 'ya'ya maza da mata, amma za su zama naku ba, domin za a kai su
bauta. 42 Tarin fāra za su mamaye dukan itatuwanku da kuma hatsin gonarku.
43 Baƙin da suke tare da ku, za su yi ta ƙaruwa, ku kuwa za ku yi ta komawa baya-
baya. 44 Za su ba ku bashi, amma ba za ku ba su bashi ba. Za su zama kai, ku kuwa
za ku zama wutsiya.
45 Dukan waɗannan la'anoni za su sauko a kanku. Za su bi ku, su same ku, sai an
hallaka ku, domin ba ku yi biyayya ga Ubangiji Allahnku, kuka kuma kiyaye umarnai
da ƙa'idodin da ya ba ku ba. 46 Za su zama alamu da al'ajabi gare ku da kuma
zuriyarku har abada. 47 Gama ba ku bauta wa Ubangiji Allahnku da farin ciki da
kuma murna a lokacin wadata ba, 48 saboda haka a cikin yunwa da ƙishirwa, cikin
tsiraici da mugun talauci, za ku bauta wa abokan gāban da Ubangiji ya aiko muku.
Zai sa karkiyar ƙarfe a wuyanku har sai ya hallaka ku ƙaf.
49 Ubangiji zai kawo al'umma daga nesa, daga iyakar duniya, ta sauko a kanku
kamar gaggafa, al'ummar da ba ku san yarenta ba, 50 al'umma mai zafin hali
wadda ba ta ba wa tsofaffi girma, kuma ba ta tausayin yara. 51 Za su cinye 'ya'yan
dabbobinku da hatsin gonarku sai an hallaka ku. Ba za su rage ko ƙwayar hatsi, ko
sabon ruwan inabi, ko mai ba, ba kuwa za a bar 'yan tumakinku ba, sai an lalatar da
ku. 52 Za su kuwa kewaye ku a dukan garuruwanku, har sai katangarku masu tsayi
wadda kuke dogara gare su, sun fāɗi ko'ina a ƙasar da Ubangiji Allahnku yake ba
ku.
53 Saboda wahalar da abokan gābanku za su gasa muku a lokacin kwanto, za ku
ci 'ya'yan cikinku, naman 'ya'yanku maza da mata waɗanda Ubangiji Allahnku ya
ba ku. 54 Kai, har da mutumin da ya fi hankali da kuma kirki a cikinku, ba zai ji
tausayi ɗan'uwansa, ko matar da yake ƙauna, ko 'ya'yansa da suka ragu ba, 55 ba
kuwa zai ba waninsu wani naman 'ya'yansa da yake ci ba. Gama dukan abin da ya
rage masa ke nan saboda wahalar da abokan gābanku za su gasa muku a lokacin da
ake kwanton wa dukan biranenku. 56 Mace mafi hankali da kuma kirki a cikinku,
kai, mafi hankali da kirki da ba ta ma karambanin taɓa ƙasa da tafin ƙafarta, za tă
hana wa mijinta da take ƙauna, da kuma ɗanta, ko 'yarta abinci. 57 A ɓoye za tă ci
mahaifar da take biyo bayan ta haihu, da 'ya'yan da za tă haifa, saboda ba ta da wani
abinci lokacin da abokan gābanku za su kewaye garuruwanku da yaƙi mai tsanani.
58 In ba ku lura kuka bi dukan kalmomi wannan doka, waɗanda an rubuta a
wannan littafi ba, ba ku kuma girmama wannan suna mai ɗaukaka da kuma mai
banrazana na Ubangiji Allahnku ba, 59 Ubangiji zai aika da annoba masu zafi a kanku
da zuriyarku, masifu masu zafi waɗanda za su daɗe, da mugayen cututtuka waɗanda
ba sa kawuwa. 60 Zai kawo muku dukan cututtukan Masar da kuke tsoro, za su kuwa
manne muku. 61 Ubangiji kuma zai kawo muku kowane irin ciwo da masifar da ba
a rubuta a cikin wannan Littafin Doka ba, har sai an hallaka ku. 62 Ku da kuke da
yawa kamar taurari a sarari za ku ragu ku zama kaɗan, domin ba ku yi biyayya ga
Ubangiji Allahnku ba. 63 Kamar yadda ya gamshi Ubangiji ya sa kuka yi arziki kuka
kuma ƙaru, haka zai gamshe shi yă lalatar yă kuma hallaka ku. Za a tumɓuke ku
daga ƙasar da kuke shiga ku mallaka.
64 Sa'an nan Ubangiji zai watsar da ku cikin dukan al'ummai, daga wannan bangon
duniya zuwa wancan. A can za ku bauta waɗansu alloli, allolin itace da na dutse,
waɗanda ko ku, ko kakanninku, ba ku sani ba. 65 A cikin waɗancan al'ummai ba
za ku sami hutu ba, ba wurin hutu wa tafin ƙafanku. A can Ubangiji zai sa fargaba
a zuciyarku, yă sa idanunku su lalace, ranku zai yi suwu. 66 Za ku yi zama cikin
damuwa kullum, cike da tsoro, dare da rana, ba tabbacin abin da zai faru da ranku.
67 Da safe za ku ce, "Da ma yamma ne!" Da yamma kuma ku ce, "Da ma safiya ce!"
Saboda tsoron da ya cika zukatanku da kuma abubuwan da idanunku za su gani.
68 Ubangiji zai komar da ku cikin jiragen ruwa zuwa Masar, tafiyar da na ce kada ku

ƙara yi. A can za ku ba da kanku don sayarwa ga abokan gābanku a matsayin bayi
maza da mata, amma ba wanda zai saye ku.

# 29

*Sabuntawar alkawari*

1 Waɗannan su ne sharuɗan alkawarin da UBANGIJI ya umarci Musa yă yi da
Isra’ilawa a Mowab, wato, ban da alkawarin da ya yi da su a Dutsen Horeb.
2 Sai Musa ya tara dukan Isra’ila, ya ce musu,

Idanunku sun ga dukan abin da UBANGIJI ya yi a Masar ga Fir’auna, ga kuma
dukan shugabanninsa da kuma ga dukan ƙasarsa. 3 Da idanunku kun ga waɗannan
gwaje-gwaje, waɗannan alamu masu banmamaki, da al’ajabai masu girma. 4 Duk
da haka har wa yau UBANGIJI bai ba ku hankalin ganewa, ko idanun da za su gani,
ko kunnuwan da za su ji ba. 5 Shekaru arba’in da na jagorance ku cikin hamada,
tufafinku ba su yage ba, haka kuwa takalman da suke a ƙafafunku. 6 Ba ku ci burodi
ba, ba ku kuwa sha ruwan inabi, ko wani abu mai sa jiri ba. Ya yi haka don ku san
cewa shi ne UBANGIJI Allahnku.
7 Sa’ad da kuka kai wannan wuri, Sihon sarkin Heshbon, da Og sarkin Bashan, suka
fito don su yi yaƙi da mu, amma muka ci su da yaƙi. 8 Muka ƙwace ƙasarsu, muka
ba da ita gādo ga mutanen Ruben, mutanen Gad, da kuma rabin mutanen Manasse.
9 Saboda haka sai ku kiyaye, ku bi sharuɗan wannan alkawari, don ku yi nasara a
cikin kome da kuke yi. 10 Yau, ga ku nan tsaye, dukanku a gaban UBANGIJI Allahnku,
shugabanninku da manyan mutanenku, dattawanku da hafsoshinku, da kuma dukan
sauran mutanen Isra’ila, 11 tare da ’ya’yanku da matanku, da baƙin da suke zama
sansanoninku, har ma da waɗanda suke muku faskare, da waɗanda suke ɗiba muku
ruwa. 12 Kuna tsaye a nan don ku yi alkawari da UBANGIJI Allahnku, alkawarin da
UBANGIJI yake yi ta wurin rantsuwa da ku a wannan rana, 13 don yă mai da ku
jama’arsa yau, shi kuwa yă zama Allahnku kamar yadda ya yi muku alkawari, da
yadda kuma ya rantse wa kakanninku, Ibrahim, Ishaku da kuma Yaƙub. 14 Ina yin
wannan alkawari da rantsuwar, ba da ku kaɗai da 15 kuke tsattsaye a nan tare da
mu a yau a gaban UBANGIJI Allahnmu ba, amma har da waɗanda ba sa nan yau.
16 Ku kanku kun san yadda muka yi zama a Masar, da yadda muka yi ta ratsawa
ta tsakiyar al’ummai muka wuce. 17 A cikinsu, kun ga siffofi masu banƙyama da
gumaka na itace da dutse, na azurfa da zinariya. 18 Kada zuciyar wani mutum, ko ta
wata mata ko na wani iyali, ko wata kabila cikinku yau, ta bar bin UBANGIJI Allahnku,
tă koma ga bauta wa gumakan waɗannan al’ummai. Kada a sami wani tushe mai ba
da ’ya’ya masu dafi, masu ɗaci a cikinku.
19 Idan kuma wani mutum ya ji kalmomi na wannan rantsuwa, ya kuma sa
wa kansa albarka yana tunani cewa, “Ba abin da zai same ni, ko da na nace a
taurinkaina.” Wannan zai jawo lalacewar dukan Isra’ila tare da kai. 20 UBANGIJI
ba zai gafarce shi ba, fushinsa da kishinsa za su ƙuna a kan wannan mutum. Dukan
la’anonin da aka rubuta a wannan littafi za su fāɗo a kansa, UBANGIJI kuwa zai shafe
sunansa daga ƙarƙashin sama. 21 UBANGIJI zai ware shi daga dukan kabilan Isra’ila
don yă hukunta shi bisa ga dukan la’anonin alkawarin da aka rubuta a wannan
Littafin Doka.
22 Tsararraki masu zuwa nan gaba, wato, ’ya’yan da za su gāje ku, da baƙon da ya
zo daga ƙasa mai nisa, za su ga annobar ƙasar, da cuce-cucen da UBANGIJI ya buge ta
da su. 23 Kasar gaba ɗaya za tă zama gishiri mai ƙuna marar amfani da kuma kibiritu,
babu shuki, babu abin da yake tsirowa, babu itatuwan da suke girma a cikinta. Za
tă zama kamar yadda aka hallaka Sodom da Gomorra, Adma da Zeboyim, waɗanda

UBANGIJI ya hallaka cikin zafin fushinsa. 24 Dukan al'ummai za su yi tambaya su
ce, "Me ya sa UBANGIJI ya yi haka da wannan ƙasa? Me ya jawo wannan fushi mai
tsanani haka?"
25 Amsar kuwa za tă zama, "Wannan ya zama haka domin wannan mutane, sun yi
watsi da alkawarin UBANGIJI Allah na kakanninsu, alkawarin da ya yi da su sa'ad da
ya fitar da su daga Masar. 26 Sun juya, suka bauta wa waɗansu alloli, suka rusuna
musu, allolin da ba su sani ba, allolin da UBANGIJI bai ba su ba. 27 Saboda haka fushin
UBANGIJI ya yi ƙuna a kan wannan ƙasa, har ya kawo dukan la'anoni da aka rubuta
a wannan littafi a kanta. 28 Cikin zafin fushi da babbar hasala UBANGIJI ya tumɓuke
su daga ƙasarsu, ya watsar da su cikin wata ƙasa dabam, kamar yadda suke a yau."
29 UBANGIJI Allahnmu bai bayyana abubuwa na yanzu da na nan gaba ba, amma
ya umarce mu mu kiyaye kalmomin dokar da ya ba mu, mu da kuma 'ya'yanmu har
abada.

# 30

### *Arziki bayan an juyo ga UBANGIJI*

1 Sa'ad da dukan albarku da la'anonin nan da na sa a gabanku suka zo muku, kuka
kuma sa su a zuciya, a duk inda UBANGIJI Allahnku ya watsar da ku a cikin al'ummai,
2 sa'ad da kuma ku da 'ya'yanku kuka komo ga UBANGIJI Allahnku, kuka kuma yi
biyayya da dukan zuciyarku da kuma dukan ranku, bisa ga kome da na umarce ku
a yau, 3 a sa'an nan ne UBANGIJI Allahnku zai yi muku jinƙai, yă ji tausayinku, yă
kuma sāke tattara ku daga dukan al'ummai inda ya warwatsa ku. 4 Ko da ma an
kore ku zuwa ƙasa mafi nisa a ƙarƙashin sammai, daga can UBANGIJI Allahnku zai
tattara ku, yă dawo da ku. 5 Zai dawo da ku zuwa ƙasar da take ta kakanninku,
za ku kuwa mallake ta. Zai sa ku yi arziki, ku kuma yi yawa fiye da kakanninku.
6 UBANGIJI Allahnku zai yi wa zukatanku kaciya da kuma zukatan zuriyarku, saboda
ku ƙaunace shi da dukan zuciyarku da kuma dukan ranku, ku kuma rayu. 7 UBANGIJI
Allahnku zai sa dukan waɗannan la'anoni a kan abokan gābanku waɗanda suke
ƙinku, suke kuma tsananta muku. 8 Za ku sāke yi wa UBANGIJI biyayya, ku kuma bi
dukan umarnan da nake ba ku a yau. 9 Sa'an nan UBANGIJI Allahnku zai mayar da
ku masu arziki ƙwarai a cikin dukan aiki hannuwanku, da kuma cikin 'ya'yanku,
da 'ya'yan shanunku, da kuma hatsin gonarku. UBANGIJI zai sāke jin daɗinku yă
sa ku yi arziki, kamar dai yadda ya ji daɗin kakanninku. 10 In dai kuka yi biyayya
ga UBANGIJI Allahnku, kuka kuma kiyaye umarnansa da ƙa'idodin da aka rubuta a
wannan Littafin Doka, kuka juyo ga UBANGIJI Allahnku da dukan zuciyarku da kuma
dukan ranku.

### *Zaɓi rai ko mutuwa*

11 To, abin da nake umartanku a yau, ba mai wuya ba ne gare ku, ba kuma abin
da ya fi ƙarfinku ba ne. 12 Ba ya can sama, balle ku ce, "Wa zai hau sama yă kawo
mana, yă kuma furta mana, don mu yi biyayya?" 13 Ba kuwa yana gaba da teku ba,
da za ku ce, "Wa zai haye tekun don yă kawo mana, yă kuma furta mana, don mu yi
biyayya?" 14 A'a, kalmar tana nan dab da ku, tana cikin bakinku da cikin zuciyarku,
don ku yi biyayya.
15 Ku duba, na sa a gabanku a yau, rai da wadata, mutuwa da kuma hallaka. 16 Gama
na umarce ku a yau, ku ƙaunaci UBANGIJI Allahnku, don ku yi tafiya a hanyoyinsa,
ku kuma kiyaye umarnansa, ƙa'idodinsa da kuma dokokinsa, sa'an nan za ku rayu,
ku kuma ƙaru, UBANGIJI Allahnku kuwa zai albarkace ku a ƙasar da kuke shiga don
ci gādonta.
17 Amma in zukatanku suka kangare, ba su kuwa yi biyayya ba, in kuma aka rinjaye
ku don ku rusuna ga waɗansu alloli ku yi musu bauta, 18 na furta muku yau cewa

tabbatacce za a hallaka ku. Ba za ku zauna a ƙasar da kuke hayewa Urdun don ku
shiga ku ci gādonta ba.
19 A wannan rana na kira bisa sama da ƙasa a matsayin shaidu a kanku, cewa na sa
a gabanku rai da mutuwa, albarku da la'anoni. Yanzu sai ku zaɓi rai, saboda ku da
'ya'yanku ku rayu 20 don kuma ku ƙaunaci Ubangiji Allahnku, ku saurari muryarsa,
ku kuma manne masa. Gama Ubangiji shi ranku, zai kuwa ba ku shekaru masu yawa
a ƙasar da ya rantse zai ba wa kakanninku, Ibrahim, Ishaku da Yaƙub.

# 31

*Yoshuwa ya gāji Musa*

1 Sai Musa ya fita ya kuma faɗa waɗannan kalmomi ga dukan Isra'ila cewa,
2 "Yanzu shekaruna ɗari da ashirin ne, ba na iya kaiwa da komowa. Ubangiji ya
ce mini, 'Ba za ka haye Urdun ba.' 3 Ubangiji Allahnku kansa zai haye a gabanku. Zai
hallaka waɗannan al'ummai da suke gabanku, za ku kuwa mallaki ƙasarsu. Yoshuwa
shi ma zai haye a gabanku, yadda Ubangiji ya faɗa. 4 Ubangiji zai yi da su, yadda
ya yi da Sihon da Og, sarakunan Amoriyawa, waɗanda ya hallaka tare da ƙasarsu.
5 Ubangiji zai bashe su gare ku, dole kuma ku yi musu dukan abin da na umarce
ku. 6 Ku ƙarfafa, ku yi ƙarfin hali. Kada ku ji tsoro, ko ku firgita saboda su, gama
Ubangiji Allahnku yana tafe tare da ku, ba zai taɓa barinku ko yă yashe ku ba."
7 Sai Musa ya kira Yoshuwa, ya ce masa a gaban dukan Isra'ila, "Ka ƙarfafa, ka
kuma yi ƙarfin hali, gama dole ka tafi tare da mutanen nan zuwa cikin ƙasar da
Ubangiji ya rantse cewa za ba wa kakanninku, dole kuma ka raba ta gare su ta zama
gādonsu. 8 Ubangiji kansa yana tafe a gabanka, zai kuma kasance tare da kai, ba zai
taɓa barinka ko yă yashe ka ba. Kada ka ji tsoro; kada kuma ka karai."

*Karantawar doka a gaban jama'a*

9 Sai Musa ya rubuta wannan doka ya kuma ba da ita ga firistoci, 'ya'yan Lawi
maza, waɗanda sukan ɗauka akwatin alkawarin Ubangiji, da kuma dukan dattawan
Isra'ila. 10 Sa'an nan Musa ya umarce su ya ce, "A ƙarshen kowace shekara bakwai, a
shekara ta yafe basususuwa, a lokacin Bikin Tabanakul, 11 sa'ad da dukan Isra'ila suka
zo, don su bayyana a gaban Ubangiji Allahnku, a wurin da zai zaɓa, za ku karanta
wannan doka a gabansu, a kunnuwansu. 12 Ku tattara mutane, maza, mata da kuma
yara, da baƙin da suke zama a cikin garuruwanku, saboda su saurara, su kuma koyi
tsoron Ubangiji Allahnku, su lura, su bi dukan kalmomin wannan doka. 13 'Ya'yansu,
waɗanda ba su san wannan doka ba, dole su ji ta, su kuma koyi tsoron Ubangiji
Allahnku muddin ranku a ƙasar da kuke haye Urdun ku ci gādonta."

*An yi faɗin tawayen Isra'ila*

14 Sai Ubangiji ya ce wa Musa, "Yanzu ranar mutuwarka ta yi kusa. Ka kira
Yoshuwa, ku shigo Tentin Sujada, inda zan ba shi ragamar aiki." Saboda haka Musa
da Yoshuwa suka zo, suka kuma shiga Tentin Sujada.
15 Ubangiji kuwa ya bayyana a Tentin Sujada a cikin ginshiƙin girgije, sai girgijen
ya tsaya a ƙofar Tentin Sujada. 16 Sai Ubangiji ya ce wa Musa, "Za ka huta tare da
kakanninka, waɗannan mutane kuwa ba da daɗewa ba za su yi karuwanci ga baƙin
alloli na ƙasar da za su shiga. Za su yashe ni su kuma karya alkawarin da na yi da
su. 17 A wannan rana zan yi fushi da su, in kuma yashe su; zan ɓoye fuskata daga
gare su, za a kuwa hallaka su. Masifu masu yawa da wahaloli masu yawa za su auka
musu, a wannan rana kuwa za su ce, 'Masifun nan sun same mu domin Allahnmu
ba ya tare da mu' 18 Tabbatacce kuwa, zan ɓoye musu fuskata saboda muguntar da
suka aikata, suka kuma bi gumaka.

19 "To, sai ka rubuta wannan waƙa domin kanka, ka koya wa Isra'ilawa, ka kuma
sa su rera ta, don tă zama shaida a kansu. 20 Sa'ad da na kawo su cikin ƙasa mai zub
da madara da zuma, ƙasar da na yi alkawari da rantsuwa ga kakanninsu, sa'ad da
kuma suka ci suka ƙoshi, suka kuma yi ƙiba, za su juya ga waɗansu alloli su bauta
musu, su ƙi ni, su kuma karya alkawarina. 21 Sa'ad da kuma masifu masu yawa
da wahaloli masu yawa suka auko musu, wannan waƙa za tă zama shaida a kansu,
domin zuriyarsu ba za tă manta da ita ba. Na san abin da za su iya yi, kafin ma in
kawo su cikin ƙasar da na yi musu alkawari da rantsuwa." 22 Sai Musa ya rubuta
wannan waƙa a wannan rana, ya kuma koya wa Isra'ilawa.

23 Ubangiji ya ba wa Yoshuwa ɗan Nun wannan umarni, "Ka ƙarfafa, ka kuma
yi ƙarfin hali, gama za ka kawo Isra'ilawa cikin ƙasar da na yi musu alkawari da
rantsuwa, ni kaina kuwa zan kasance tare da kai."

24 Bayan Musa ya gama rubuta kalmomin dokan nan a littafi daga farko zuwa
ƙarshe, 25 sai ya ba wa Lawiyawa, waɗanda suke ɗaukar akwatin alkawarin Ubangiji
wannan umarni, 26 "Ku ɗauki wannan Littafin Doka ku sa shi kusa da akwatin
alkawarin Ubangiji Allahnku. A can zai kasance a matsayin shaida a kanku. 27 Gama
na sani yadda kuke 'yan tawaye da masu taurinkai. In kuna yin tawaye ga Ubangiji
tun ina da rai tare da ku, yaya tawayen da za ku yi masa bayan na rasu! 28 Ku tattara
dukan dattawan kabilanku, da kuma dukan hafsoshinku a gabana, saboda in faɗa
waɗannan kalmomi a kunnuwansu, in kuma kira ga sama da ƙasa su zama shaida
a kansu. 29 Gama na san cewa bayan rasuwata, tabbatacce za ku lalace gaba ɗaya,
ku juye daga hanyar da na umarce ku. A kwanaki masu zuwa, masifa za tă auka
muku saboda za ku aikata mugunta a gaban Ubangiji, ku tsokane shi har yă yi fushi
ta wurin abin da hannuwanku suka yi."

### *Waƙar Musa*

30 Sai Musa ya karanta kalmomin waƙar daga farko zuwa ƙarshe a kunnuwan
dukan taron jama'ar Isra'ila.

## 32

1 Ku saurara, ya ku sammai, zan yi magana;
bari duniya ta ji maganar bakina.
2 Bari koyarwata tă zubo kamar ruwan sama
kalmomina kuma su sauko kamar raɓa,
kamar yayyafi a kan sabuwar ciyawa,
kamar ruwan sama mai yawa a kan tsirai marasa ƙarfi.

3 Zan yi shelar sunan Ubangiji.
Ku yabi girman Allahnmu!
4 Shi Dutse ne, ayyukansa cikakku ne,
dukan hanyoyinsa kuwa masu adalci ne.
Allah mai aminci, wanda ba ya yin rashi gaskiya,
shi mai adalci ne, nagari ne kuma.

5 Sun aikata mugunta a gabansa;
saboda abin kunyarsu, su ba 'ya'yansa ba ne,
amma wata muguwar tsara ce, karkatacciya.
6 Haka za ku biya Ubangiji,
Ya ku wawaye da kuma mutane marasa hikima?
Shi ba Ubanku ba ne, Mahaliccinku,
wanda ya yi ku, ya kuma siffanta ku?

7 Ku tuna da kwanakin dā,
ku tuna da tsararrakin da suka wuce tun tuni,
Ku tambayi iyayenku, za su faɗa muku,
dattawanku, za su kuma bayyana muku.
8 Sa'ad da Mafi Ɗaukaka ya ba da al'ummai gādonsu,
sa'ad da ya raba dukan 'yan adam,
ya kafa iyakoki wa mutane
bisa ga yawan 'ya'yan Isra'ila maza.
9 Gama rabon UBANGIJI shi ne mutanensa,
Yaƙub shi ne rabon gādonsa.

10 A cikin hamada ya same shi,
a jeji marar amfani, inda namomi suke kuka.
Ya tsare shi, ya kuma lura da shi;
ya bi da shi kamar ƙwayar idonsa,
11 kamar gaggafar da take yawo a kan sheƙarta
tana rufe 'ya'yanta,
ta buɗe fikafikanta don tă kwashe su
tă ɗauke su a kafaɗunta.
12 UBANGIJI kaɗai ya jagorance shi;
babu wani baƙon gunkin da yake tare da shi.

13 Ya sa shi ya hau ƙwanƙolin dutse
ya ciyar da shi da amfanin gona.
Ya shayar da shi da zuma daga dutse,
da kuma mai daga dutsen ƙanƙara,
14 da kindirmo da madara daga shanu da tumaki
da ƙibabbun tumaki da awaki,
da zaɓaɓɓun ragunan Bashan
da kuma ƙwayoyin alkama mafi kyau.
Ka sha ruwan inabi ja wur mai kumfa.

15 Yeshurun* ya yi ƙiba, ya yi kauri;
cike da abinci, ya zama da nauyi, ya kuma zama sumul.
Ya yashe Allahn da ya yi shi,
ya ƙi Dutse Cetonsa.
16 Suka sa shi kishi saboda baƙin allolinsu,
suka husata shi da gumakan banƙyamarsu.
17 Suka yi hadaya ga aljanu, waɗanda ba Allah ba,
ga allolin da ba su sani ba,
ga allolin da aka shigo da su daga baya,
allolin da kakanninku ba su ji tsoronsu ba.
18 Kuka rabu da Dutsen da ya zama mahaifi gare ku;
kuka manta da Allahn da ya haife ku.

19 UBANGIJI ya ga wannan ya kuma ƙi su,
domin 'ya'yansa maza da mata sun husata shi.
20 Ya ce, "Zan ɓoye fuskata daga gare su,
in ga ƙarshensu;
gama su muguwar tsara ce,

* **32:15** Yeshurun yana nufin mai adalci, wato, Isra'ila.

’ya’ya ne marasa aminci.
21 Sun sa ni kishi ta wurin abin da ba allah ba,
suka kuma husata ni da gumakansu na wofi.
Zan sa su yi kishi ta wurin waɗanda ba mutane ba;
zan sa su yi fushi ta wurin al’ummar da ba ta da sani.
22 Gama fushina ya kama wuta,
tana ci har ƙurewar zurfin lahira.
Za tă cinye duniya da girbinta,
tă kuma sa wuta a tussan duwatsu.

23 “Zan tula masifu a kansu
in kuma gama kibiyoyina a kansu.
24 Zan aika da yunwa mai tsanani a kansu,
zazzaɓi mai zafi da muguwar annoba;
zan aika da haƙoran namun jeji a kansu,
da dafin mesa masu ja da ciki.
25 Waɗanda suke a waje, takobi zai kashe su,
a cikin gidajensu kuma tsoro zai mamaye su.
’Yan maza da ’yan mata za su hallaka,
haka ma jarirai da maza masu furfura.
26 Na ce zan watsar da su
in sa a manta da su a tunanin ’yan adam.
27 Amma ina tsoron tsokanar abokin gāba,
don kada abokan gāba su kāsa ganewa
har su ce, ‘Hannunmu ne ya yi nasara;
ba Ubangiji ne ya aikata dukan wannan ba.’ ”

28 Al’ummai ne marasa azanci,
babu ganewa a cikinsu.
29 A ce su masu hikima ne har su gane wannan
su gane abin da ƙarshensu zai zama!
30 Yaya mutum guda zai kore dubu,
mutum biyu su sa dubu goma su gudu,
sai ko Dutsensu ya sayar da su,
sai ko Ubangiji ya bashe su.
31 Gama dutsensu ba kamar Dutsenmu ba ne,
abokan gābanmu sun san da haka.
32 Kuringarsu ta fito daga kuringar Sodom ne,
daga gonakin Gomorra kuma.
’Ya’yan inabinsu dafi ne,
nonnansu masu ɗaci ne.
33 Ruwan inabinsu dafin macizai ne,
mugun dafin gamshaƙa ne.

34 “Ban jibge wannan a ma’ajiya
na kuma yimƙe shi a taskokina ba?
35 Sakayya nawa ne, zan kuwa ɗau fansa.
A cikin lokaci, ƙafarsu za tă yi santsi;
ranar masifarsu ta yi kusa
hallakarsu kuma tana gaggautawa a kansu.”

36 UBANGIJI zai shari'anta mutanensa
yǎ kuma ji tausayin bayinsa
sa'ad da ya ga ƙarfinsu ya ƙare
babu kowa kuma da ya rage, bawa ko 'yantacce.
37 Zai ce, "To, ina allolinsu,
dutsen da suka yi mafaka a ciki,
38 allolin da suka ci kitsen hadayunsu
suka kuma sha ruwan inabin hadayunsu?
Ku sa su tashi su taimake ku mana!
Bari su ba ku mafaka!

39 "Ku duba yanzu cewa ni ne Shi!
Ba wani allah in ban da ni.
Nakan kashe in kuma rayar,
nakan sa rauni in kuma warkar,
ba wanda yake da iko yǎ cece wani daga hannuna.
40 Na ɗaga hannu sama na kuma furta.
Muddin ina raye har abada,
41 sa'ad da na wasa takobi mai walƙiya
hannuna kuwa ya cafke shi don yin hukunci,
zan ɗau fansa a kan abokan gābana
in sāka wa waɗanda suke ƙina.
42 Zan sa kibiyoyina su bugu da jini,
yayinda takobina yana cin nama,
jinin kisassu da na kamammu,
kawunan shugabannin abokan gāba."

43 Ku yi farin ciki, ya ku al'ummai, tare da mutanensa,†
gama zai rama ɗau fansar jinin bayinsa;
zai ɗau fansa a kan abokan gābansa
yǎ kuma yi kafara domin ƙasarsa da mutanensa.
44 Sai Musa ya zo da Yoshuwa‡ ɗan Nun suka faɗa dukan waɗannan kalmomi
wannan waƙa a kunnen mutane. 45 Sa'ad da Musa ya gama karanta waɗannan
kalmomi ga dukan Isra'ila, 46 ya ce musu, "Ku riƙe dukan kalmomin da na furta muku
a yau, don ku umarce 'ya'yanku su lura, su yi biyayya da dukan kalmomin wannan
doka. 47 Ba kalmomi kurum ba ne dominku, amma har ranku ma. Ta wurinsu za ku
yi tsawon rai a ƙasar da kuke haye Urdun ku ci gādonta."

### *Musa ya mutu a kan Dutsen Nebo*

48 A wannan rana UBANGIJI ya ce wa Musa, 49 "Ka hau Duwatsun Abarim zuwa
Dutsen Nebo a Mowab, tsallake daga Yeriko, ka hangi Kan'ana, ƙasar da nake ba
wa Isra'ilawa gādo. 50 A can kan dutsen da ka hau za ka mutu a kuma tara ka
ga mutanenka, kamar yadda ɗan'uwanka Haruna ya mutu a Dutsen Hor aka kuma
tara shi ga mutanensa. 51 Wannan kuwa domin ku biyu kun fid da aminci gare ni a
gaban Isra'ilawa a ruwan Meriba ta Kadesh, a Hamadar Zin kuma saboda ba ku riƙe
tsarkina a cikin Isra'ilawa ba. 52 Saboda haka, za ka ga ƙasar daga nesa kawai; ba za
ka shiga ƙasar da nake ba wa mutanen Isra'ila ba."

† **32:43** Ko kuwa Ku sa mutanensa su yi farin ciki, ya al'ummai ‡ **32:44** Da Ibraniyanci Hosheya, wani sunan Yoshuwa.

# 33

*Musa ya albarkaci kabilu*

1 Wannan ita ce albarkar da Musa mutumin Allah ya furta a kan Isra’ilawa, kafin
yă rasu. 2 Ya ce,
“Ubangiji ya zo daga Sinai
ya haskaka a bisansu daga Seyir;
ya haskaka daga Dutsen Faran.
Ya zo tare da dubban tsarkakansa
daga kudu, daga gangara dutsensa.
3 Tabbatacce kai ne wanda yake ƙaunar mutane;
dukan tsarkaka suna a hannunka.
A ƙafafunka, duk suka rusuna,
daga wurinka kuma suka karɓi umarni,
4 dokar Musa ta ba mu dokoki,
mallakar taron Yaƙub.
5 Shi ne sarki a bisa Yeshurun
sa’ad da shugabannin mutane suka taru,
tare da kabilan Isra’ila.

6 “Bari Ruben yă rayu, kada yă mutu,
kada* mutanensa su zama kaɗan.”
7 Ya kuma faɗa wannan game da Yahuda,
“Ka ji, ya Ubangiji, kukan Yahuda;
ka kawo shi wurin mutanensa.
Da hannuwansa ya kāre kansa.
Ka taimake shi a kan maƙiyansa!”
8 Game da Lawi ya ce,
“Tummim da Urim na
mutumin da ka nuna masa tagomashi ne.
Ka gwada shi a Massa;
ka yi faɗa da shi a ruwan Meriba.
9 Ya yi zancen mahaifinsa da mahaifiyarsa ya ce,
‘Ban kula da su ba.’
Bai gane da ’yan’uwansa ba,
ko yă yarda da ’ya’yansa,
amma ya kiyaye maganarka
ya tsare alkawarinka.
10 Ya koyar da farillanka ga Yaƙub,
dokarka kuma ga Isra’ila.
Ya miƙa turare a gabanka
da kuma hadaya ta ƙonawa ɗungum a kan bagadenka.
11 Ka albarkaci ɗaukan dabarunsa, ya Ubangiji,
ka kuma ji daɗin aikin hannuwansa.
Ka murƙushe kwankwaso waɗanda suka tayar masa;
ka bugi abokan gābansa har sai ba su ƙara tashi ba.”
12 Game da Benyamin ya ce,
“Bari ƙaunataccen Ubangiji yă zauna lafiya kusa da shi,
gama yana tsare shi dukan yini,
wanda kuma Ubangiji yake ƙauna yana zama a tsakanin kafaɗunsa.”
13 Game da Yusuf ya ce,

* **33:6** Ko kuwa amma bari

“Bari UBANGIJI yă albarkaci ƙasarsa
da raɓa mai daraja daga sama a bisa
da kuma zurfin ruwan da suke kwance a ƙarƙashi;
14 da abubuwa masu kyau da rana take kawo,
da kuma abubuwa mafi kyau da wata zai iya haifar;
15 da zaɓaɓɓun kyautai na daɗaɗɗun duwatsu,
da kyawawan amfani na madawwaman tuddai.
16 Tare da kyautai mafi kyau na duniya da cikarta,
da tagomashi na wanda yake zama a ƙaramin itace mai ƙonewa.
Bari duk waɗannan su zauna a kan Yusuf,
a goshin sarki a cikin ’yan’uwansa.
17 Cikin daraja yana yi kamar ɗan fari na bijimi;
ƙahoninsa ƙahonin ɓauna ne.
Tare da su zai tukwiyi al’ummai,
har ma da waɗanda suke ƙarshen duniya.
Haka dubu dubban Efraim suke;
haka dubban Manasse suke.”
18 Game da Zebulun ya ce,
“Ka yi farin ciki, Zebulun, a fitowarka,
kai kuma Issakar, a cikin tentunanka.
19 Za su kira mutane zuwa dutse,
a can za su miƙa hadayun adalci;
za su yi biki a yalwan tekuna,
a dukiyoyin da aka ɓoye a cikin yashi.”
20 Game da Gad ya ce,
“Mai albarka ne wanda ya fadada mazaunin Gad!
Gad yana zama a can kamar zaki,
yana yayyage a hannu da kai.
21 Ya zaɓi ƙasa mafi kyau wa kansa;
aka ajiye masa rabon shugaba.
Sa’ad da shugabannin mutane suka taru,
ya aikata adalcin UBANGIJI
da kuma hukuncinsa game da Isra’ila.”
22 Game da Dan ya ce,
“Dan ɗan zaki ne,
yana tsalle daga Bashan.”
23 Game da Naftali ya ce,
“Naftali ƙosasshe ne da tagomashin UBANGIJI,
ya kuma cika albarkarsa;
zai gāji gefen kudu zuwa tafki.”
24 Game da Asher ya ce,
“Mafi albarka na ’ya’yan, shi ne Asher;
bari yă sami tagomashi daga ’yan’uwansa,
bari kuma yă wanke ƙafafunsa a cikin mai.
25 Madogaran ƙofofinka za su zama ƙarfe da tagulla,
ƙarfinka kuma zai zama daidai da kwanakinka.

26 “Babu wani kamar Allah na Yeshurun,
wanda yake hawa a bisa sammai don yă taimake ka
a kan gizagizai kuma a cikin darajarsa.
27 Allah madawwami shi ne mafakarka,

a ƙarƙashina kuma madawwamin hannuwa ne.
Zai kore abokin gābanka a gabanka,
yana cewa, 'Ka hallaka shi!'
28 Haka Isra'ila zai zauna lafiya shi kaɗai;
zuriyar Yaƙub a tsare
a ƙasar hatsi da sabon ruwan inabi,
inda sammai za su zuba raɓa.
29 Kai mai albarka ne, ya Isra'ila!
Wane ne yake kamar ka,
mutanen da UBANGIJI ya ceta?
Shi ne mafakarka da mai taimakonka
da kuma takobinka mai ɗaukaka.
Abokan gābanka za su zo neman jinƙai a gabanka,
za ka kuwa tattake masujadansu."†

# 34

*Mutuwar Musa*

1 Sai Musa ya hau Dutsen Nebo daga filayen Mowab, zuwa ƙwanƙolin Fisga, wanda
yake ƙetare Yeriko. A can UBANGIJI ya nuna masa dukan ƙasar, daga Gileyad zuwa
Dan, 2 da ta dukan Naftali, da yankin Efraim da na Manasse, dukan ƙasar Yahuda har
zuwa Bahar Rum,* 3 da Negeb da dukan yankin Kwarin Yeriko, Birnin Dabino, har
zuwa Zowar. 4 Sa'an nan UBANGIJI ya ce masa, "Wannan ce ƙasar da na yi alkawari da
rantsuwa wa Ibrahim, Ishaku da Yaƙub, sa'ad da na ce, 'Zan ba da ita ga zuriyarku.'
Na bar ka ka gani da idanunka, amma ba za ka haye zuwa cikinta ba."
5 Nan fa, a ƙasar Mowab Musa bawan UBANGIJI ya mutu, yadda UBANGIJI ya faɗa.
6 Aka binne shi† a Mowab, a kwarin kusa da Bet-Feyor, amma har wa yau babu wanda
ya san inda kabarinsa yake. 7 Musa yana da shekara ɗari da ashirin sa'ad da ya mutu,
duk da haka idanunsa ba su dushe ba, ƙarfinsa kuwa bai ragu ba. 8 Isra'ilawa suka
yi makoki domin Musa a filayen Mowab kwana talatin, sai da lokacin kuka, da na
makoki suka ƙare.
9 To, Yoshuwa ɗan Nun ya cika da ruhun hikima, gama Musa ya ɗibiya hannuwansa
a kansa. Saboda haka Isra'ilawa suka saurare shi, suka kuma aikata abin da UBANGIJI
ya umarci Musa.
10 Tun daga nan ba a sāke yin wani annabi a Isra'ila kamar Musa ba, wanda
UBANGIJI ya san shi fuska da fuska, 11 wanda kuma ya yi dukan waɗannan alamu
banmamaki da al'ajaban da UBANGIJI ya aike shi yă yi a Masar, da a kan Fir'auna,
da a kan dukan shugabanninsa, da kuma a kan dukan ƙasarsa. 12 Gama babu wani
wanda ya taɓa nuna iko mai ƙarfi, ko yă aikata ayyukan banrazana waɗanda Musa
ya yi a gaban dukan Isra'ila.

† **33:29** Ko kuwa za ka yi tafiya a kan jikunansu * **34:2** Wato, Mediterraniyan. † **34:6** Ko kuwa Aka binne shi

# Yoshuwa

*UBANGIJI ya umarci Yoshuwa*

1 Bayan mutuwar Musa bawan UBANGIJI, sai UBANGIJI ya ce wa Yoshuwa ɗan Nun,
mataimakin Musa, 2 “Bawana Musa ya mutu. Yanzu sai ka tashi tare da mutanen nan
duka, ku yi shirin ƙetare kogin Urdun zuwa cikin ƙasar da zan ba su Isra’ilawa. 3 Zan
ba ku duk ƙasar da za ku taka, kamar yadda na yi wa Musa alkawari. 4 Kasar da
ta kama daga hamada zuwa Lebanon, zuwa babban Kogin, wato, Kogin Yuferites, da
dukan ƙasar Hittiyawa zuwa Bahar Rum, wajen yamma. 5 Ba wanda zai yi tsayayya
da kai dukan kwanakin ranka. Yadda na kasance tare da Musa, haka zan kasance
tare da kai; ba zan taɓa rabuwa da kai ba; ba zan yashe ka ba.
6 “Ka yi ƙarfin hali ka kuma kasance da rashin tsoro, gama kai za ka bi da mutanen
nan har su karɓi ƙasar da na yi wa kakanninsu alkawari zan ba su. 7 Ka yi ƙarfin hali
ka kuma kasance da rashin tsoro, ka yi lura fa, ka yi biyayya da dokokin da bawana
Musa ya ba ka; kada ka kauce ga bin dokokin ko hagu ko dama, domin ka yi nasara
a duk, inda za ka je. 8 Kada ka bar Littafin Dokokin nan yă rabu da bakinka, sai dai
ka yi ta tunani game da shi dare da rana, don ka lura, ka yi duk abin da aka rubuta a
ciki, ta haka ne za ka yi nasara cikin duk abin da za ka yi. 9 Ba ni na umarce ka ba?
Ka yi ƙarfin hali ka kuma kasance da rashin tsoro. Kada ka ji tsoro; kada ka karaya,
gama UBANGIJI Allahnka zai kasance tare da kai duk inda za ka je.”
10 Saboda haka sai Yoshuwa ya umarci shugabannin mutane, 11 “Ku ratsa cikin
sansani, ku gaya wa mutane, ‘Ku shirya guzurinku. Nan da kwana uku za ku ƙetare
Urdun a nan, don ku je ka mallaki ƙasar da UBANGIJI Allahnku yake ba ku ta zama
taku.’ ”
12 Amma Yoshuwa ya ce wa mutanen Ruben, mutanen Gad da kuma rabin mutanen
kabilar Manasse, 13 “Ku tuna da umarnin da Musa bawan UBANGIJI ya yi muku.
‘UBANGIJI Allahnku ya ba ku hutawa, ya kuma ba ku wannan ƙasa.’ 14 Matanku,
da yaranku, da kuma dabbobinku za su kasance a ƙasar da Musa ya ba ku a
gabashin Urdun, amma dole mayaƙanku, su yi shirin yaƙi su haye, su yi gaba tare
da ’yan’uwanku, za ku taimaki ’yan’uwanku 15 har sai lokacin da UBANGIJI ya ba su
hutawa, kamar yadda ya yi muku, kuma har sai su ma sun ƙwace ƙasar da UBANGIJI
Allahnku ya yi alkawari zai ba su. Bayan haka ne za ku koma ku mallaki ƙasarku,
wadda Musa bawan UBANGIJI ya ba ku a gabashin Urdun.”
16 Sai suka amsa wa Yoshuwa suka ce, “Duk abin da ka ce mu yi, za mu yi. Duk
inda kuma ka aike mu, za mu je. 17 Kamar yadda muka yi wa Musa biyayya, haka za
mu yi maka biyayya. UBANGIJI Allahnka ya kasance tare da Musa. 18 Duk wanda ya
yi wa maganarka tawaye, ya ƙi yă yi biyayya da maganarka, ko da umarnin da ka ba
shi, za a kashe shi. Ka dai ƙarfafa ka kuma yi ƙarfi hali!”

## 2

*Rahab da ’yan leƙen asiri*

1 Sai Yoshuwa ɗan Nun ya aika ’yan leƙen asiri guda biyu a ɓoye daga Shittim ya
ce, “Ku je ku duba, ku ga yadda wurin yake, musamman Yeriko.” Sai suka je suka
shiga gidan wata karuwa mai suna Rahab, suka sauka a can.
2 Aka gaya wa sarkin Yeriko cewa, “Ji fa, waɗansu Isra’ilawa sun shigo nan da
dare don su leƙi asirin ƙasar.” 3 Saboda haka sai sarki ya aika wannan saƙo zuwa
ga Rahab, “Ki fito da mutanen da suka zo suka sauka a gidanki, gama sun zo su leƙi
asirin ƙasar ne gaba ɗaya.”

4 Amma matar ta ɓoye mutanen nan biyu. Ta ce, “I, mutanen sun zo wurina, amma
ban san daga ina suka zo ba, 5 da yamma kuwa, kafin a rufe ƙofar gari sai mutanen
suka tafi. Ban san hanyar da suka bi ba, ku yi sauri ku bi su. Mai yiwuwa ku same
su.” 6 (Amma ta kai su saman rufin ɗaki ta ɓoye su a ƙarƙashin karan rama da ta
baza a rufin ɗaki.) 7 Sai mutanen garin suka kama hanyar Urdun don su nemi ’yan
leƙen asirin, daga fitar su sai aka rufe ƙofar garin.
8 Kafin ’yan leƙen asirin su kwanta, sai ta tafi wurinsu a bisa rufin ɗakin 9 ta ce
musu, “Na sani UBANGIJI ya riga ya ba ku ƙasan nan, tsoronku kuma ya kama mu
har zukatan mazaunan ƙasar duka sun narke saboda ku. 10 Mun ji yadda UBANGIJI ya
busar da ruwan Jan Teku domin ku lokacin da kuka fito daga ƙasar Masar, da kuma
abin da kuka yi wa Sihon da Og, sarakunan nan biyu na Amoriyawa gabas da Urdun,
waɗanda kuka hallaka su sarai. 11 Da muka ji labarin, duk sai zuciyar kowa ta narke,
kowa ya karaya saboda ku, gama UBANGIJI Allahnku shi ne Allah na sama da ƙasa.
12 Yanzu ina roƙonku ku rantse mini da UBANGIJI cewa za ku yi wa iyalina alheri
kamar yadda na yi muku alheri. Ku ba ni ƙwaƙƙwarar shaida cewa 13 za ku ceci
rayukan mahaifina da mahaifiyata, da ’yan’uwana maza da mata, da duk waɗanda
suke nasu, za ku cece mu daga mutuwa.”
14 Mutanen suka tabbatar mata suka ce, “Ranmu a bakin ranki! In ba ki faɗa wa
kowa abin da ya kawo mu ba, za mu yi miki alheri da aminci lokacin da UBANGIJI ya
ba mu ƙasar.”
15 Sai ta zura igiya ta taga suka bi, domin gidan da take yana haɗe da katangar
birnin. 16 Ta ce musu, “Ku tafi cikin tuddan ƙasar don kada mutanen sarki su same
ku. Ku ɓuya a can na kwana uku, har sai masu nemanku su komo, sa’an nan ku
kama hanyarku.”
17 Mutanen suka ce mata, “Rantsuwar da kika sa muka yi, ba za tă yi amfani ba 18 sai
in kin ɗaura jan ƙyalle a tagar da kika zura mu, kuma sai in kin kawo mahaifinki da
mahaifiyarki, da ’yan’uwanki, da dukan iyalinki cikin gidanki. 19 In wani ya fita kan
hanya, alhakin jininsa yă kasance a kansa; ba ruwanmu. Amma in aka taɓa wani da
yake cikin gidanki tare da ke, alhakin jininsa yana kanmu. 20 In kika tone mana asiri,
za mu karya alkawarin da kika sa muka yi.”
21 Ta ce, “Na yarda! Bari yă zama yadda kuka ce.”
Sai ta sallame su suka tafi. Ta kuwa ɗaura jan ƙyalle a tagar.
22 Sai suka tafi, suka shiga cikin tuddai, suka yi zamansu a can kwana uku har masu
nemansu suka koma, gama masu nemansu suka yi ta nema ko’ina a hanyar, amma
ba su sami kowa ba. 23 Sa’an nan mutanen nan biyu, ’yan leƙen asiri suka sauka
daga tuddai suka haye kogi zuwa wurin Yoshuwa ɗan Nun, suka gaya masa duk abin
da ya faru da su. 24 Suka ce wa Yoshuwa, “Ba shakka UBANGIJI ya ba mu ƙasan nan
duka, tana hannunmu, mutane can duk sun narke da tsoro saboda mu.”

# 3

*Ketare kogin Urdun*

1 Kashegari Yoshuwa da dukan Isra’ilawa suka tashi daga Shittim suka nufi Urdun
inda suka sauka kafin su haye. 2 Bayan kwana uku sai shugabannin suka zazzaga
sansani, suna 3 ba da umarni ga mutane, suna cewa, “Lokacin da kuka ga akwatin
alkawari na UBANGIJI Allahnku, da firistoci waɗanda su ne Lawiyawa, suna ɗauke da
shi, sai ku tashi daga inda kuke, ku bi shi. 4 A ta haka za ku san inda za ku bi, gama
ba ku taɓa bin hanyar ba. Sai dai ku ɗan ba da rata wajen yadi ɗari tara tsakaninku
da akwatin alkawari, kada ku kusace shi.”
5 Yoshuwa ya ce wa mutane, “Ku tsarkake kanku, gama gobe UBANGIJI zai yi
abubuwan al’ajabi a cikinku.”

6 Yoshuwa ya ce wa firistoci, “Ku ɗauki akwatin alkawari ku sha gaba.” Sai suka
ɗauki akwatin alkawari suka wuce gaban sauran jama’a.

7 Ubangiji kuwa ya ce wa Yoshuwa, “Yau, zan fara ɗaukaka ka a gaban Isra’ilawa
duka don su sani cewa ina tare da kai kamar yadda na kasance tare da Musa. 8 Ka
ce wa firistoci waɗanda suke ɗauke da akwatin alkawari, ‘Sa’ad da kuka kai bakin
Urdun, ku shiga cikin ruwan ku tsaya.’ ”

9 Yoshuwa ya ce wa Isra’ilawa, “Ku zo nan ku ji maganar Ubangiji Allahnku. 10 Ta
haka ne za ku san cewa Allah mai rai yana tare da ku, kuma ba shakka a gabanku
za ku gani zai kore Kan’aniyawa, Hittiyawa, Hiwiyawa, Ferizziyawa, Girgashiyawa,
Amoriyawa da Yebusiyawa. 11 Ku duba, akwatin alkawarin Ubangiji na dukan duniya
zai yi gaba cikin Urdun kafin ku. 12 Yanzu sai ku zaɓi mutum goma sha biyu daga
kabilan Isra’ila, ɗaya daga kowace kabila. 13 Kuma da firistoci waɗanda suke ɗauke
da akwatin alkawarin Ubangiji, Ubangiji dukan duniya, sun sa ƙafa cikin ruwan kogin
Urdun, ruwan da yake gudu a rafin zai tsaya cik yă taru a wuri ɗaya.”

14 Saboda haka sa’ad da mutanen suka tashi don su ƙetare Urdun, firistocin da
suke ɗauke da akwatin alkawarin suka sha gaba. 15 Da kaka Urdun yakan cika makil
da ruwa. Duk da haka da zarar firistoci masu ɗauke da akwatin alkawari suka tsoma
ƙafafunsu a gefen ruwa, 16 sai ruwan da yake gangarowa ya tsaya, ya tattaru a wuri
ɗaya ya yi tudu daga nan har zuwa wani garin da ake kira Adam kusa da Zaretan,
ruwan da yake gangarowa zuwa Tekun Araba (Tekun Gishiri) kuma ya yanke gaba
ɗaya. Sai mutane suka ƙetare kusa da Yeriko. 17 Firistocin kuwa da suke ɗauke
da akwatin alkawarin Ubangiji suka tsaya daram a kan busasshiyar ƙasa a tsakiyar
Urdun a lokacin da Isra’ilawa suka ƙetarewa, har sai da dukan mutane suka gama
ƙetarewa.

# 4

1 Da al’umma gaba ɗaya suka ƙetare Urdun, Ubangiji ya ce wa Yoshuwa, 2 “Ka zaɓi
mutum goma sha biyu daga cikin mutane, ɗaya daga kowace kabila, 3 ka ce musu
kowa yă ɗauki dutse ɗaya daga tsakiyar Urdun daidai inda firistoci suka tsaya, ku
kai su, ku ajiye a inda za ku sauka yau.”

4 Sai Yoshuwa ya kira mutum goma sha biyu da ya zaɓa daga cikin Isra’ilawa,
ɗaya daga kowace kabila 5 ya ce musu, “Ku je tsakiyar Urdun inda akwatin alkawari
na Ubangiji Allahnku yake. Kowannenku yă ɗauki dutse ɗaya a kafaɗarsa, bisa ga
yawan kabilan Isra’ila, 6 yă zama muku alama. Nan gaba in yaranku suka tambaye
ku suka ce, ‘Mece ce ma’anar kasancewar duwatsun nan a nan?’ 7 Sai ku ce musu,
ruwan Urdun ya yanke a gaban akwatin alkawari na Ubangiji, a lokacin da akwatin
alkawarin ya ƙetare Urdun. Waɗannan duwatsu za su zama abin tuni ga Isra’ilawa
har abada.”

8 Isra’ilawa kuwa suka yi yadda Yoshuwa ya umarce su. Suka ɗauki duwatsu guda
goma sha biyu bisa ga yawan kabilan Isra’ila, yadda Ubangiji ya gaya wa Yoshuwa;
suka tafi da su masauƙinsu, a can suka ajiye su. 9 Yoshuwa ya ɗora duwatsu goma
sha biyun a tsakiyar Urdun daidai inda firistoci waɗanda suke ɗauke da akwatin
alkawarin Ubangiji suka tsaya. Suna nan a can har wa yau.

10 Firistocin da suke ɗauke da akwatin alkawari suka tsaya a tsakiyar Urdun,
har aka gama dukan abin da Ubangiji ya umarci Yoshuwa yă gaya wa mutane,
kamar yadda Musa ya ce Yoshuwa yă yi. Mutanen suka wuce da sauri. 11 Sai da
dukan mutanen suka wuce sa’an nan akwatin alkawari da firistoci suka sha gaba.
12 Mutanen Ruben, Gad da rabin kabilar Manasse suka ƙetare da shirin yaƙi, suka
wuce gaban Isra’ila kamar yadda Musa ya ce su yi. 13 Wajen mutum dubu arba’in
shirye domin yaƙi, suka wuce a gaban Ubangiji zuwa filayen Yeriko.

14 A ranan nan UBANGIJI ya ɗaukaka Yoshuwa a gaban Isra'ilawa; suka kuma ba shi girma dukan kwanakin ransa, kamar yadda suka girmama Musa.
15 Sa'an nan UBANGIJI ya ce wa Yoshuwa, 16 "Ka umarci firistocin da suke ɗauke da akwatin Shaida su fito daga cikin Urdun."
17 Sai Yoshuwa ya umarci firistoci ya ce, "Ku fito daga cikin Urdun."
18 Firistocin kuwa suka fito daga kogin ɗauke da akwatin alkawarin UBANGIJI. Nan da nan da ƙafafunsu suka taɓa busasshiyar ƙasa, sai ruwan Urdun ya gangaro ya cika kogin kamar yadda yake a dā.
19 A rana ta goma ga wata na farko, mutane suka haura daga Urdun suka sauka a Gilgal a gabashin iyakar Yeriko. 20 Sai Yoshuwa ya kafa duwatsu goma sha biyun
nan da suka ɗauko daga Urdun. 21 Ya ce wa Isra'ilawa, "Nan gaba in yaranku
suka tambayi iyayensu suka ce, 'Mece ce ma'anar waɗannan duwatsun?' 22 Ku ce
musu, 'Isra'ilawa sun ƙetare kogin Urdun a kan busasshiyar ƙasa.' 23 Gama UBANGIJI Allahnku ya sa ruwan Urdun ya yanke a gabanku, har sai da kuka gama wucewa, kamar yadda ya yi a Jan Teku, a lokacin da ya busar da shi a gabanmu har sai da muka gama wucewa. 24 Ya yi wannan ne domin dukan mutanen duniya su san cewa UBANGIJI mai iko ne, domin kuma ku zama masu tsoron UBANGIJI Allahnku."

# 5

### *Kaciya a Gilgal*

1 To, da dukan sarakunan Amoriyawa na yammancin Urdun, da dukan sarakunan Kan'aniyawan da suke bakin teku suka ji yadda UBANGIJI ya busar da kogin Urdun a gaban Isra'ilawa, har sai da dukansu suka ƙetare, zuciyarsu ta narke, suka karaya sosai har ma suka rasa samun ƙarfin hali su fuskanci Isra'ilawa.
2 A lokacin nan UBANGIJI ya ce wa Yoshuwa, "Ka yi wuƙaƙe na duwatsu ka yi wa
Isra'ilawa kaciya." 3 Sai Yoshuwa ya yi wuƙaƙe na duwatsu, ya yi wa Isra'ilawa kaciya a Gibeyat-Ha'aralot.
4 Dalilin da ya sa ya yi haka shi ne, dukan waɗanda suka fito daga Masar, dukan mazan da suka kai shekarun shiga soja, sun mutu a cikin jeji a hanya bayan sun
bar Masar. 5 Dukan mutanen da suka fito daga Masar an yi musu kaciya, amma duk
waɗanda aka haifa a jeji a tafiya daga Masar, ba a yi musu ba. 6 Isra'ilawa sun yi tafiya a jeji shekaru arba'in, har sai da dukan mazan da suka kai shekarun shiga soja da suka bar Masar suka mutu, domin ba su yi wa UBANGIJI biyayya ba. Gama UBANGIJI ya rantse cewa ba zai bar su su ga ƙasar da ya yi wa iyayensu alkawari da rantsuwa cewa zai ba su ba, ƙasar da zuma da madara suke kwarara, ƙasar da take cike da
albarka. 7 Sai ya sa yaransu ne suka taso a maimakonsu, su ne waɗanda Yoshuwa ya
yi wa kaciya. Sun kasance ba kaciya gama ba a yi musu ba a hanya. 8 Kuma bayan da aka yi wa al'ummar kaciya dukansu, sai suka dakata a nan, sai da suka warke.
9 Sai UBANGIJI ya ce wa Yoshuwa, "Yau na kawar muku da zargin Masar." Saboda haka ake kiran sunan wurin Gilgal har wa yau.
10 Da yamman rana ta goma sha huɗu ga wata, lokacin da suke a Gilgal a filin Yeriko,
Isra'ilawa suka yi Bikin Ketarewa. 11 A kashegarin Bikin, a wannan rana, sai suka
ci daga cikin amfanin ƙasar, burodi marar yisti da hatsin da aka gasa. 12 Kashegari bayan da suka ci amfanin ƙasar kuwa, Manna ta yanke, mutanen Isra'ila kuma ba su ƙara samunta ba. A wannan shekara suka fara cin amfanin ƙasar Kan'ana.

### *Fāɗuwar Yeriko*

13 To, da Yoshuwa ya yi kusa da Yeriko, ya tā da idanunsa ya duba, sai ya ga wani mutum tsaye a gabansa riƙe da takobi, sai Yoshuwa ya je wurinsa ya ce masa, "Kai namu ne ko na abokan gābanmu?"

14 Mutumin ya ce, “Babu ko ɗaya, na dai zo ne a matsayin shugaban rundunar
sojojin UBANGIJI.” Sai Yoshuwa ya kwanta da fuskarsa har ƙasa, ya girmama shi, ya
ce masa, “Ranka yă daɗe, wane saƙo kake da shi domin bawanka?”
15 Shugaban rundunar sojojin UBANGIJI ya amsa ya ce, “Ka cire takalmanka, gama
wurin da kake tsaye, mai tsarki ne.” Sai Yoshuwa ya cire takalmansa.

# 6

1 Kofofin Yeriko kuwa a kulle suke ciki da waje saboda Isra’ilawa, ba mai fita babu
kuma mai shiga.
2 Sai UBANGIJI ya ce wa Yoshuwa, “Duba, na ba ka nasara a kan Yeriko, duk da
sarkinta da mayaƙanta. 3 Da kai da dukan sojoji, ku zaga birnin sau ɗaya kullum.
Ku yi haka har kwana shida. 4 Ka sa firistoci guda bakwai su riƙe ƙahoni raguna su
kasance a gaban akwatin alkawari. A rana ta bakwai sai ku zaga birnin sau bakwai,
firistocin suna busa ƙahoni. 5 Sa’ad da kuka ji sun ɗauki dogon lokaci suna busa
ƙaho, sai mutane gaba ɗaya su tā da murya su yi ihu da ƙarfi; katangar birnin kuwa
za tă rushe, sai sojoji su haura, ko wanne yă nufi inda ya fuskanta kai tsaye.”
6 Yoshuwa ɗan Nun kuwa ya kira firistoci ya ce musu, “Ku ɗauki akwatin alkawari,
ku sa firistoci guda bakwai su riƙe ƙahoni su kasance a gabansa.” 7 Sai ya umarci
jama’a ya ce, “Mu je zuwa! Ku zaga birnin, masu tsaro da makamai su shiga gaban
akwatin alkawarin UBANGIJI.”
8 Da Yoshuwa ya gama yin wa mutane magana, sai firistoci guda bakwai waɗanda
suke riƙe da ƙahoni guda bakwai a gaban UBANGIJI suka sha gaba suna busa
ƙahoninsu, akwatin alkawari kuwa yana biye da su. 9 Masu tsaro da makamai kuma
suna gaban firistoci waɗanda suke busa ƙahoni, masu tsaro daga baya kuma suna
bin akwatin alkawari, ana ta busa ƙahoni. 10 Amma Yoshuwa ya umarci mutane ya
ce, “Kada ku yi kururuwar yaƙi, kada ku tā da murya, kada ku ce kome, sai ranar
da na ce ku yi ihu, a sa’an nan ne sai ku yi ihu!” 11 Sai ya sa aka ɗauki akwatin
alkawarin UBANGIJI aka kewaye birnin da shi sau ɗaya, sa’an nan mutane suka dawo
masauƙinsu suka kwana a can.
12 Kashegari, Yoshuwa ya tashi da sassafe, firistoci kuma suka ɗauki akwatin
alkawarin UBANGIJI. 13 Firistoci guda bakwai waɗanda suke riƙe da ƙahoni guda
bakwai suka shiga gaba, suna takawa a gaban akwatin alkawarin UBANGIJI suna kuma
busa ƙahoni, masu tsaro ɗauke da makamai suna gabansu, sai masu tsaro da suke
baya suna biye da akwatin alkawarin UBANGIJI. 14 A rana ta biyu suka sāke zaga
birnin sau ɗaya, suka kuma koma masauƙinsu. Haka suka yi har kwana shida.
15 A rana ta bakwai, suka tashi da sassafe suka zaga birnin sau bakwai yadda suka
saba. A wannan rana kaɗai ne suka zaga birnin sau bakwai. 16 A zagawa ta bakwai,
da firistoci suka busa ƙahoni, sai Yoshuwa ya ba sojojin umarni ya ce, “Ku yi ihu,
gama UBANGIJI ya ba ku birnin! 17 Birnin da dukan abin da yake cikinta za a miƙa
su ga UBANGIJI. Rahab karuwan nan kaɗai ce, da dukan waɗanda suke tare da ita a
gidanta za a bari da rai domin ta ɓoye ’yan leƙen asirin ƙasa da muka aika. 18 Amma,
ba za ku ɗauki wani abin da za a hallaka ba, idan kuka yi haka, za ku jawo masifa
da hallaka a kan mutanen Isra’ila a inda kuka sauka. 19 Dukan azurfa da zinariya,
da kwanonin tagulla da na ƙarfe, keɓaɓɓu ne ga UBANGIJI, dole a sa su cikin ma’ajin
UBANGIJI.”
20 Da aka busa ƙahoni, sojoji suka yi ihu, da jin ƙarar ƙahoni, mutane suka kuma
yi ihu, sai katangar ta rushe; dukan mutanen kuwa suka shiga birnin kai tsaye, suka
yi nasara a kanta. 21 Suka miƙa wa UBANGIJI birnin, suka hallaka kowane abu mai
ran da yake cikin birnin da takobi, maza da mata, yara da tsofaffi, shanu, tumaki da
jakuna.

22 Yoshuwa ya ce wa mutanen nan biyu waɗanda suka je leƙen asirin ƙasar, “Ku
shiga gidan karuwan nan ku fitar da ita da duk waɗanda suke nata bisa ga alkawarin
da kuka yi mata.” 23 Sai samarin waɗanda suka je leƙen asirin suka shiga suka fitar da
Rahab, mahaifinta da mahaifiyarta, da ’yan’uwanta da duk abin da yake nata. Suka
fitar da iyalinta gaba ɗaya suka sa su a wani wuri, ba a cikin masauƙin Isra’ilawa ba.
24 Sa’an nan suka ƙona birnin tare da dukan abin da yake ciki tatas, amma suka sa
azurfa da zinariya da kayan tagulla da na ƙarfe a cikin ma’aji na haikalin UBANGIJI.
25 Amma Yoshuwa ya bar Rahab karuwan nan bai kashe ta ba, ita da iyalinta da duk
abin da yake nata, domin ita ta ɓoye mutanen da Yoshuwa ya aika Yeriko don su leƙo
asirin ƙasar kuma ta zauna tare da Isra’ilawa har wa yau.
26 A lokacin nan Yoshuwa ya yi wannan alkawari cewa, “UBANGIJI zai tsine wa
mutumin da zai yi ƙoƙarin sāke gina birnin nan, Yeriko.

“A bakin ran ɗan farinsa
zai kafa harsashin birnin;
a bakin ran ɗan autansa kuma
zai sa ƙofofin birnin.”

27 UBANGIJI ya kasance tare da Yoshuwa, aka kuma san da shi a duk fāɗin ƙasar.

# 7

*Zunubin Akan*

1 Amma Isra’ilawa ba su yi aminci game da kayan da aka hallaka ba; Akan ɗan
Karmi, ɗan Zabdi, ɗan Zera, na kabilan Yahuda ya kwashi waɗansu abubuwa, saboda
haka fushin UBANGIJI ya sauka a kan Isra’ilawa.
2 Sai Yoshuwa ya aika mutane daga Yeriko zuwa Ai kusa da Bet-Awen gabas da
Betel, ya ce musu, “Ku je ku leƙo ku ga yadda yankin yake.” Sai mutanen suka je
suka leƙo asirin ƙasar Ai.
3 Da suka dawo wurin Yoshuwa suka ce, “Ba lalle dukan jama’a su je yaƙi da Ai ba,
ka aika mutum dubu biyu ko dubu uku su je su ciwo ƙasar da yaƙi, ba sai ka dami
mutane duka ba, gama mutanen wurin kaɗan ne.” 4 Saboda haka sai kimanin mutum
duba uku suka haura; amma mutanen Ai suka fatattake su, 5 suka kashe Isra’ilawa
wajen mutum talatin da shida, suka fafari Isra’ilawa tun daga bakin ƙofar birnin har
zuwa wurin da ake fasa duwatsu. Suka karkashe su a gangare. Wannan ya sa zuciyar
Isra’ilawa ta narke suka zama kamar ruwa.
6 Sai Yoshuwa ya yaga tufafinsa ya fāɗi rubda ciki a gaban akwatin alkawarin
UBANGIJI, yana can har yamma. Dattawan Isra’ila ma suka yi haka, suka zuba toka
a kawunansu. 7 Yoshuwa kuma ya ce, “Ya UBANGIJI Mai Iko Duka, me ya sa ka sa
mutanen nan suka ƙetare Urdun don ka bari mu shiga hannun Amoriyawa su hallaka
mu? Kila da mun haƙura mun zauna a ɗaya gefen Urdun da ya fi mana! 8 Ya UBANGIJI
me zan ce, yanzu da abokan gāban Isra’ilawa suka ci ƙarfinsu? 9 Yanzu Kan’aniyawa
da sauran jama’a za su ji, za su zo su kewaye mu su share sunanmu daga duniya. To,
yanzu me za ka yi don girman sunanka?”
10 UBANGIJI ya ce wa Yoshuwa, “Ka tashi! Me kake yi kwance rubda ciki?
11 Isra’ilawa sun yi zunubi, sun karya sharaɗin da na yi musu. Sun ɗauki waɗansu
abubuwan da aka keɓe; sun yi sata, sun yi ƙarya, sun ɓoye su cikin kayansu. 12 Shi
ne ya sa Isra’ilawa suka kāsa yin tsayayya da abokan gābansu; suka juya suka gudu
domin za a hallaka su. Ba zan sāke kasancewa tare da ku ba sai in kun hallaka duk
abin da aka keɓe don hallaka.
13 “Tashi, ka je ka tsarkake mutane. Ka ce musu su tsarkake kansu, su yi shiri domin
gobe; gama ga abin da UBANGIJI, Allah na Isra’ila ya ce, a cikinku akwai abubuwan
da aka keɓe, ya Isra’ilawa. Ba za ku iya yin tsayayya da abokan gābanku ba sai in
kun rabu da abubuwan nan da aka haramta.

14 “ ‘Da safe ku zo kabila-kabila. Kabilar da UBANGIJI ya ware, za tă zo gaba gida-
gida; gidan da UBANGIJI ya ware, za su zo gaba iyali-iyali. Iyalin kuma da UBANGIJI
ya ware, za su zo gaba mutum bayan mutum. 15 Mutumin da aka same shi da
haramtattun abubuwan kuwa za a ƙone shi, duk da mallakarsa domin ya karya
sharaɗin da UBANGIJI ya yi muku, ya yi abin kunya a Isra’ila!’ ”

16 Kashegari da sassafe Yoshuwa ya sa Isra’ilawa suka fito kabila-kabila, aka ware
kabilar Yahuda. 17 Gidan Yahuda suka zo gaba, sai aka ware gidan Zera, aka sa suka
fito iyali-iyali, sai aka ware Zabdi. 18 Yoshuwa kuwa ya sa iyalin Zabdi suka fito
mutum-mutum, sai kuwa aka ware Akan ɗan Karmi, ɗan Zimri, ɗan Zera na kabilar
Yahuda.

19 Sai Yoshuwa ya ce wa Akan, “Dana, sai ka ba UBANGIJI, Allah na Isra’ila ɗaukaka,
ka yi masa yabo. Ka gaya mini abin da ka yi; kada ka ɓoye mini.”

20 Akan kuwa ya amsa ya ce, “Gaskiya ne! Na yi wa UBANGIJI, Allah na Isra’ila
zunubi. Ga abin da na yi. 21 A cikin ganimar, na ga doguwar riga mai kyau irin ta
Babilon, da shekel ɗari biyu na azurfa, da kuma sandan zinariya mai nauyin shekel
hamsin, sai raina ya so su, na kuwa kwashe su. Na tona rami a cikin ƙasa a tentina;
na ɓoye.”

22 Sai Yoshuwa ya aiki ’yan aika suka tafi da gudu zuwa tenti ɗin, haka kuwa suka
same su a ɓoye a tentinsa, da azurfa a ƙarƙashi. 23 Suka kwashe kayan daga tenti
ɗin suka kawo wa Yoshuwa da sauran Isra’ilawa, suka baza su a gaban UBANGIJI.

24 Sai Yoshuwa da dukan Isra’ilawa suka ɗauki Akan ɗan Zera, da azurfar, doguwar
rigar, sandan zinariya, ’ya’yansa maza da mata, shanunsa, jakuna da tumaki, tentinsa
da duk abin da yake da shi, suka kai su Kwarin Akor. 25 Yoshuwa ya ce, “Me ya sa ka
jawo mana wahala haka? UBANGIJI zai kawo maka wahala kai ma a yau.”

Sai dukan Isra’ilawa suka jajjefe shi, bayan da suka gama jifarsa sai suka ƙone
sauran. 26 Suka tara manyan duwatsu a kan Akan, tarin duwatsun na nan a can har
wa yau. Sa’an nan UBANGIJI ya huce daga fushinsa mai zafi. Saboda haka ake kiran
wurin Kwarin Akor.

# 8

### *An hallaka Ai*

1 Sai UBANGIJI ya ce wa Yoshuwa, “Kada ka ji tsoro; kada ka karaya. Ka ɗauki dukan
sojojin ku kai wa Ai hari, gama na ba ka nasara a kan sarkin Ai, mutanensa, birninsa
da kuma ƙasarsa. 2 Za ku yi wa Ai yadda kuka yi wa Yeriko da sarkinta, sai dai za
ku kwashe ganima da dabbobinta su zama naku. Ku yi kwanto a bayan birnin.”

3 Yoshuwa da dukan sojojin suka fita su kai wa Ai hari. Sai ya zaɓi sojojinsa
waɗanda suka fi saura duka iya yaƙi guda dubu talatin, ya tura su da dad dare 4 ya
ba su umarni ya ce, “Ku ji da kyau, za ku yi kwanto a bayan birnin, kada ku yi nisa
da birnin. Kowannenku yă kasance a faɗake. 5 Ni da waɗanda suke tare da ni za
mu nufi birnin, a lokacin da mutanen suka taso mana yadda suka yi dā, sai mu guje
musu. 6 Za su bi mu har su yi nisa da birnin, gama za su ce, ‘Suna gudu kamar yadda
suka yi dā.’ Saboda haka lokacin da muka guje musu, 7 sai ku tashi daga inda kuka yi
kwanto, ku ci birnin da yaƙi, UBANGIJI Allahnku zai ba da shi a hannunku. 8 Lokacin
da kuka ƙwace birnin, sai ku sa masa wuta. Ku yi abin da UBANGIJI ya umarta. Ku
tabbata kun yi abubuwan da na ce.”

9 Sai Yoshuwa ya sallame su, suka kuma tafi wurin da za su yi kwanto, suka kwanta
suna fako tsakanin Betel da Ai, yamma da Ai, amma Yoshuwa ya kwana tare da
mutanen.

10 Kashegari da sassafe Yoshuwa ya tattara mutanensa, sai shi da shugabannin
Isra’ilawa suka sha gaba suka taka zuwa Ai. 11 Dukan sojojin da suke tare da shi suka

nufi birnin, da suka kai kuwa sai suka kafa sansaninsu a arewancin Ai. Tsakaninsu
da Ai akwai kwari. 12 Yoshuwa ya sa mutum dubu biyar suka yi kwanto tsakanin
Betel da Ai, a yammancin birnin. 13 Mutanen suka kafa sansaninsu arewa da birnin,
sansani na ʼyan kwanto kuwa yana yamma da birnin, amma Yoshuwa ya kwana a
kwarin.
14 Saʼad da sarkin Ai ya ga haka, shi da duk mutanen birnin suka hanzarta da
sassafe don su gamu da Israʼilawa, su yi yaƙi da su a wani wurin da yake fuskantar
Araba. Amma bai san cewa an yi masa kwanto a bayan birnin ba. 15 Yoshuwa da
duk Israʼilawa suka bari aka fafare su, sai suka gudu zuwa cikin jeji. 16 Aka kira duk
mazan Ai su fafare su, suka kuwa fafari Yoshuwa, aka yaudare su suka yi nisa da
birnin. 17 Ba namijin da ya rage a Ai ko Betel da bai fita don yǎ fafari Israʼilawa ba.
Suka bar birnin a buɗe, suka tafi fafarar Israʼilawa.
18 Sai Ubangiji ya ce wa Yoshuwa, "Ka riƙe māshin da yake hannunka ka nuna
wajen Ai, gama zan ba da birnin a hannunka." Yoshuwa kuwa ya miƙa māshin ta
wajen Ai. 19 Da yin haka kuwa sai mutanen da suka yi kwanto suka tashi nan da nan
daga inda suke, suka nufi birnin a guje, suka shiga suka ci birnin da yaƙi, suka kuma
cinna mata wuta da sauri.
20 Mutanen Ai suka juya suka ga hayaƙin birninsu yana tashi sama, amma ba yadda
za su iya tsira ta koʼina, gama Israʼilawan da suke gudu zuwa cikin jeji suka juya suka
fara fafarar waɗanda suke fafararsu. 21 Lokacin da Yoshuwa da dukan Israʼilawa suka
ga waɗanda suka yi kwanto sun ci birnin da yaƙi, hayaƙi kuwa ya cika birnin, sai
suka juya suka kai wa mutanen Ai hari. 22 Mutanen da suka yi kwanto su ma suka
fito daga birnin suka tasar musu, ya zama an kama su a tsakiya, ga Israʼilawa daga
kowane gefe. Israʼilawa kuwa suka karkashe su duka ba su bar wani da rai ba, ba
kuma wanda ya tsere. 23 Amma suka tafi da sarkin Ai da rai suka kawo shi wurin
Yoshuwa.
24 Da Israʼilawa suka gama kashe duk mutanen Ai a filaye da kuma a cikin jeji
inda suka fafare su, kuma da aka karkashe kowane mutumin Ai da takobi sai dukan
Israʼilawa suka koma Ai suka karkashe duk waɗanda suke cikinsa. 25 A ranan nan,
dukan mutanen Ai da aka kashe, mutum dubu goma sha biyu ne maza da mata.
26 Gama Yoshuwa bai janye hannunsa da yake riƙe da māshinsa ba har sai da ya
hallaka dukan mazaunan Ai. 27 Amma Israʼilawa suka kwashe ganima da dabbobin
birnin nan yadda Ubangiji ya umarci Yoshuwa.
28 Yoshuwa kuwa ya ƙone Ai, ya mai da ita tarin ƙasa, ta zama kufai har wa yau.
29 Ya rataye sarkin Ai a kan itace, ya bar shi a can har yamma. Da rana ta faɗi,
Yoshuwa ya umarta a ɗauke gawar sarkin a jefa a gaban ƙofar birnin. Suka kuma
tara manyan duwatsu a kan gawar, tsibin na nan har wa yau.

### *An sabunta yarjejjeniya a Dutsen Ebal*
### *(Maimaitawar Shariʼa 27.1-26)*

30 Yoshuwa kuwa ya yi wa Ubangiji, Allah na Israʼila bagade a Dutsen Ebal, 31 kamar
yadda Musa bawan Ubangiji ya umarci Israʼilawa. Ya gina bisa ga abin da yake a
rubuce a cikin Littafin Dokoki na Musa, bagade na duwatsun da ba a sassaƙa su
ba, waɗanda ba wani ƙarfen da ya taɓa su. Suka miƙa wa Ubangiji hadayu na
ƙonawa da hadayu na salama a kai. 32 A can, a gaban Israʼilawa, Yoshuwa ya rubuta
dokokin Musa a kan duwatsun. 33 Sai Israʼilawa duka, da baƙi, da haifaffun gida,
da dattawansu, da shugabanninsu, da alƙalansu, suka tsaya a gefe-gefen akwatin
alkawarin Ubangiji, suna fuskantar waɗanda suke ɗauke da shi, wato, firistoci
waɗanda su ne Lawiyawa. Rabin mutanen suka tsaya a gaban Dutsen Gerizim,
rabinsu kuma suka tsaya a gaban Dutsen Ebal, kamar yadda Musa bawan Ubangiji
ya riga ya umarta, cewa su sa wa mutanen Israʼilawa albarka.

34 Bayan haka, Yoshuwa ya karanta duk abin da yake a cikin Dokoki, albarku da
la'anoni, kamar yadda suke a rubuce a cikin Littafin Dokoki. 35 Babu wata kalmar
da Musa ya umarta da Yoshuwa bai karanta wa dukan taron Isra'ilawa ba, haɗe da
mata, da yara, da baƙin da suke zama tare da su.

# 9

*Ruɗun da mutanen Gibeyon suka yi*

1 To, sa'ad da dukan sarakunan yammancin Urdun suka ji waɗannan abubuwa,
sai waɗanda suke kan tudu, da na cikin kwari a yammanci, da dukan waɗanda
suke gefen Bahar Rum har zuwa Lebanon (sarakunan Hittiyawa, Amoriyawa,
Kan'aniyawa, Ferizziyawa, Hiwiyawa da Yebusiyawa) 2 suka haɗa kansu don su yaƙi
Yoshuwa da Isra'ila.

3 Amma da mutanen Gibeyon suka ji abin da Yoshuwa ya yi wa Yeriko da Ai, 4 sai
suka shirya wata dabara ta ruɗu, suka shirya ɗan abinci don tafiya, suka ɗauki
tsofaffin buhuna a kan jakunansu da tsofaffin salkuna na ruwan inabi, yagaggu da
suka sha ɗinki. 5 Suka sa tsofaffin takalman da suka sha gyara, suka sa tsofaffin tufafi.
Dukan abincinsu na tafiya ya bushe ya yi fumfuna. 6 Sai suka je wurin Yoshuwa a
sansanin Gilgal suka ce masa da mutanen Isra'ila, "Daga ƙasa mai nisa muka fito,
yanzu fa, sai ku yi alkawari da mu."

7 Mutanen Isra'ila kuwa suka ce wa Hiwiyawa, "Wataƙila kuna kusa da mu, ta yaya
za mu yi alkawari da ku?"

8 Suka ce wa Yoshuwa, "Mu bayinku ne."

Amma Yoshuwa ya tambaye su ya ce, "Ku wane ne, kuma daga ina kuka zo?"

9 Suka amsa suka ce, "Bayinka sun zo ne daga ƙasa mai nisa gama Ubangiji
Allahnka ya yi suna sosai. Gama mun ji labarin abubuwan da ya yi. Dukan abubuwan
da ya yi a Masar 10 da kuma duk abubuwan da ya yi wa sarakuna biyu na Amoriyawa
gabas da Urdun, Sihon sarkin Heshbon, da Og sarkin Bashan wanda ya yi mulki a
Ashtarot. 11 Dattawanmu da duk mazaunan ƙasar, suka ce mana, 'Ku ɗauki abincin
tafiyar da za ku riƙe; ku je ku same su ku ce musu, "Mu bayinku ne, ku yi alkawari
da mu." ' 12 Abincin tafiyan nan namu yana da ɗumi lokacin da muka kintsa tashi
daga gida a ranar da za mu kama hanya zuwa wurinku. Amma yanzu duba yadda
ya bushe, ya yi fumfuna. 13 Waɗannan salkuna kuma da muka cika ruwan inabi,
sababbi ne amma duba yadda suka yayyage. Tufafinmu da takalmanmu duk sun
yayyage don doguwar tafiya."

14 Mutanen Isra'ila suka ɗiba daga cikin abincin tafiyar amma ba su nemi nufin
Ubangiji ba. 15 Sa'an nan Yoshuwa ya yi alkawari zaman salama da su, cewa ba zai
kashe su ba, sai shugabannin mutanen Isra'ila kuwa suka tabbatar musu da haka ta
wurin yin rantsuwa.

16 Kwana uku bayan sun yi alkawari da Gibeyonawa, sai Isra'ilawa suka ji cewa
Gibeyonawa maƙwabtansu ne, waɗanda suke zaune kurkusa da su. 17 Saboda haka
Isra'ilawa suka tashi a rana ta uku suke je biranen mutanen, wato, Gibeyon, Kefira,
Beyerot da Kiriyat Yeyarim. 18 Amma Isra'ilawa ba su kai musu hari ba domin
shugabanninsu sun rantse musu da sunan Ubangiji, Allah na Isra'ila.

Mutane Isra'ila duka kuwa suka yi gunaguni a kan shugabannin. 19 Amma
shugabanni suka amsa musu suka ce, "Mun rantse musu da sunan Ubangiji, Allah na
Isra'ila, saboda haka ba za mu taɓa su ba yanzu. 20 Ga abin da za mu yi musu, za mu
bar su da rai don kada fushin Allah yǎ sauka a kanmu gama mun riga mun rantse
musu." 21 Suka ƙara da cewa, "Mu bar su da rai, amma bari su zama masu yankan
itace da masu ɗibo mana ruwa." Haka shugabannin suka cika alkawarinsu.

22 Yoshuwa kuwa ya aika aka kira Gibeyonawa ya ce musu, “Don me kuka ruɗe
mu kuka ce, ‘Mun zo ne daga wuri mai nisa,’ bayan kuwa kuna nan kurkusa da mu?
23 Yanzu ku la’anannu ne. Ba za ku daina zama mana masu yankan itace da kuma
masu ɗebo ruwa domin haikalin Allahnmu ba.”
24 Suka amsa wa Yoshuwa suka ce, “An gaya wa bayinka dalla-dalla yadda UBANGIJI
Allahnka ya umarci bawansa Musa yă ba ka ƙasar duka, ka kuma kashe duk masu
zama a cikinta, muka ji tsoro cewa za ka kashe mu shi ya sa muka yi haka. 25 Yanzu,
a hannunka muke, ka yi duk abin da ka ga ya yi maka kyau.”
26 Yoshuwa kuwa ya cece su daga hannun Isra’ilawa, har ba su kashe su ba. 27 A
ranar Yoshuwa ya sa Gibeyonawa suka zama masu yankan itace da ɗebo ruwa wa
jama’ar Isra’ila da kuma domin haikalin UBANGIJI a inda UBANGIJI zai zaɓa. Abin da
suke ke nan har wa yau.

# 10

*Rana ta tsaya cik*

1 Adoni-Zedek sarkin Urushalima ya ji cewa Yoshuwa ya ci Ai da yaƙi ya kuma
hallaka ta sarai, ya yi wa Ai da sarkinta abin da ya yi wa Yeriko da sarkinta, mutanen
Gibeyon kuwa sun yi yarjejjeniya ta salama da Isra’ilawa, suna kuma zama kusa da
su. 2 Shi da mutanensa suka ji tsoron wannan sosai, gama Gibeyon muhimmiyar birni
ce, har ma kamar ɗaya daga cikin biranen sarauta, ya ma fi Ai girma, mazanta duka
kuwa mayaƙa ne na ƙwarai. 3 Saboda haka sai Adoni-Zedek sarkin Urushalima ya
roƙi Hoham sarkin Hebron, Firam sarkin Yarmut, Yafiya sarkin Lakish da Debir sarki
Eglon ya ce, 4 “Ku zo ku taimake ni in kai wa Gibeyon hari. Domin sun yi yarjejjeniya
ta salama da Yoshuwa da Isra’ilawa.”
5 Sai sarakunan nan biyar na Amoriyawa, sarakunan Urushalima, Hebron, Yarmut,
Lakish da Eglon suka haɗa sojojinsu. Suka je dukansu suka yi shirin kai wa Gibeyon
hari.
6 Sai mutanen Gibeyon suka aika zuwa wurin Yoshuwa a sansani a Gilgal, “Kada ka
juya wa bayinka baya, ka zo da sauri ka cece mu! Ka taimake mu domin sarakunan
Amoriyawa duka daga kan tudu sun haɗa ƙarfinsu tare za su tasar mana.”
7 Saboda haka Yoshuwa ya tashi da rundunarsa duka, tare da dukan jarumawansa.
8 UBANGIJI ya ce wa Yoshuwa, “Kada ka ji tsoronsu; na ba ka su a hannunka. Ba
waninsu da zai iya tsayayya da kai.”
9 Bayan sun yi tafiya dukan dare daga Gilgal, Yoshuwa ya auko musu ba labari.
10 UBANGIJI ya sa suka ruɗe a gaban Isra’ilawa, Isra’ilawa kuwa suka yi babbar nasara
a kansu a Gibeyon. Isra’ilawa suka fafare su a kan hanyar zuwa Bet-Horon suka
karkashe su duka har zuwa Azeka da Makkeda. 11 Suna guje wa Isra’ilawa suna
gangarawa a kan hanyar Bet-Horon har zuwa Azeka, sai UBANGIJI ya turo manyan
duwatsu daga sararin sama suka karkashe su, waɗanda manyan duwatsun suka
kashe sun fi waɗanda Isra’ilawa suka kashe da takobi.
12 A ranar da UBANGIJI ya ba da Amoriyawa a hannun Isra’ilawa, Yoshuwa ya ce
wa UBANGIJI a gaban Isra’ilawa,

“Ke rana, ki tsaya cik a Gibeyon
Kai wata, ka je Kwarin Aiyalon.”

13 Sai rana ta tsaya cik,
wata kuma ya tsaya,
har sai da al’ummar ta ɗauki fansa
a kan abokan gābanta,
kamar yadda aka rubuta a cikin littafin Yashar.

Rana ta tsaya a sararin sama, ba tă fāɗi ba har kusan yini guda. 14 Ba a taɓa ganin
abu haka ba ko dā can, ranar da UBANGIJI ya saurari mutum. Ba shakka UBANGIJI
yana yaƙi domin Isra'ilawa.
15 Sai Yoshuwa ya koma sansanin Gilgal tare da dukan Isra'ilawa.

### *An kashe sarakunan Amoriyawa guda biyar*

16 Sarakunan guda biyar suka gudu, suka ɓuya a cikin kogo a Makkeda. 17 Lokacin
da aka gaya wa Yoshuwa cewa an sami sarakunan nan biyar a ɓoye a cikin kogo a
Makkeda. 18 Sai ya ce, "Ku mirgina manyan duwatsu ku rufe bakin kogon, sai ku
sa waɗannan mutane su yi tsaron kogon. 19 Amma kada ku tsaya a can! Ku fafari
abokan gābanku, ku kai musu hari ta baya, kada ku bari su kai biranensu, gama
UBANGIJI Allahnku ya ba da su a hannunku."
20 Saboda haka Yoshuwa da Isra'ilawa suka hallaka su da yawa ƙwarai, amma
'yan kaɗan ɗin da suka rage suka tsere zuwa cikin biranensu masu kāriya. 21 Dukan
rundunar kuma suka dawo sansanin Makkeda tare da Yoshuwa, ba abin da ya same
su. Ba wanda ya sāke tsokanar Isra'ilawa.
22 Yoshuwa ya ce, "Ku buɗe bakin kogon ku kawo mini sarakunan nan guda biyar."
23 Sai suka kawo sarakunan biyar daga cikin kogo; sarakunan Urushalima, Hebron,
Yarmut, Lakish da Eglon. 24 Sa'ad da aka kawo sarakunan nan wurin Yoshuwa, ya
kira dukan Isra'ilawa ya ce wa shugabannin rundunoni waɗanda suke tare da shi,
"Ku zo nan ku taka wuyan sarakunan nan." Sai suka zo suka taka wuyansu.
25 Yoshuwa ya ce musu, "Kada ku ji tsoro, ko kuwa ku razana, amma ku ƙarfafa,
ku yi ƙarfin hali. Haka UBANGIJI zai yi da duk abokan gāban da za ku yi yaƙi da
su." 26 Sai Yoshuwa ya karkashe waɗannan sarakuna guda biyar, ya kuma rataye
kowannensu a bisa itace inda jikunansu suka kasance har yamma.
27 Da yamma Yoshuwa ya ba da umarni a sauko da su daga itatuwan a jefa su cikin
kogon da suka ɓuya. Aka sa manyan duwatsu aka rufe bakin kogon, suna a can har
wa yau.
28 A ranan nan Yoshuwa ya ci Makkeda da yaƙi. Ya karkashe mutanen tare da
sarkinta. Bai bar wani da rai ba. Ya yi wa sarkin Makkeda yadda ya yi wa sarkin
Yeriko.

### *An ci biranen kudu da yaƙi*

29 Sai Yoshuwa da dukan Isra'ilawa suka tashi daga Makkeda zuwa Libna, suka kai
mata hari. 30 UBANGIJI kuma ya ba da ƙasar da sarkinta a hannun Yoshuwa. Yoshuwa
ya karkashe kowa ya hallaka birnin, bai bar wani da rai ba. Ya kuma yi wa sarkin
yadda ya yi wa sarkin Yeriko.
31 Sai Yoshuwa da dukan Isra'ilawa suka tashi daga Libna zuwa Lakish; suka yi
shiri suka kai mata hari. 32 UBANGIJI ya ba da Lakish a hannun Isra'ilawa, a rana ta
biyu kuwa Yoshuwa ya ci nasara a kansu. Ya karkashe duk mutanen birnin ya kuma
hallaka birnin, kamar yadda ya yi a Libna. 33 Horam sarkin Gezer kuwa ya zo don yă
taimaki Lakish, amma Yoshuwa ya haɗa duk da shi da rundunarsa ya ci su da yaƙi,
har bai bar waninsu da rai ba.
34 Yoshuwa kuwa da dukan Isra'ilawa suka tashi daga Lakish zuwa Eglon; suka yi
shiri suka kai mata hari. 35 A ranan nan suka ci ƙasar da yaƙi, suka buge ta, suka
karkashe kowa da takobi kamar dai yadda suka yi a Lakish.
36 Sai Yoshuwa da dukan Isra'ilawa suka tashi daga Eglon zuwa Hebron suka kai
hari a can. 37 Suka ci birnin da yaƙi, suka karkashe mazaunanta, da sarkin, har da
ƙauyukan, ba wanda ya tsira kamar yadda ya yi wa Eglon. Ya hallakar da ita sarai
duk da kowane mutum da yake cikinta.

[38] Yoshuwa da Isra’ilawa duka suka juya suka kai wa Debir hari, [39] suka hallaka
birnin, da sarkinta da ƙauyukanta, suka karkashe dukan mazaunan wurin, ba su bar
wani da rai ba. Suka yi wa Debir da sarkinta yadda suka yi wa Libna da sarkinta da
kuma Hebron.
[40] Yoshuwa ya cinye yankin duka da yaƙi, haɗe da na kan tudu, da Negeb, da
kwarin yamma, da filayen cikin duwatsu tare da sarakunansu duka. Bai bar wani
da rai ba, ya kashe duk wani mai numfashi, yadda UBANGIJI, Allah na Isra’ilawa ya
umarta. [41] Yoshuwa ya ci su da yaƙi daga Kadesh Barneya zuwa Gaza, da kuma
daga dukan yankin Goshen zuwa Gibeyon. [42] Yoshuwa kuwa ya cinye sarakunan nan
duka da ƙasashensu gaba ɗaya gama UBANGIJI, Allah na Isra’ila ne ya yi yaƙi domin
Isra’ilawa.
[43] Yoshuwa kuwa ya dawo da dukan Isra’ilawa zuwa sansani a Gilgal.

# 11

*An ci sarakunan arewa da yaƙi*

[1] Sa’ad da Yabin sarkin Hazor ya ji wannan, sai ya aika saƙo zuwa wurin Yobab
sarkin Madon, da sarkin Shimron, da Akshaf, [2] ya kuma aika zuwa ga sarakunan
arewa waɗanda suke kan tuddai da kuma waɗanda suke cikin Araba a kudancin
Kinneret da cikin filayen kwari, da cikin Nafot Dor a yamma; [3] ya kuma aika zuwa
ga Kan’aniyawa a gabas da yamma; da kuma zuwa ga Amoriyawa, Hittiyawa da
Ferizziyawa, da Yebusiyawa da suke kan tuddai; da kuma Hiwiyawa masu zama a
gindin dutsen Hermon a yankin Mizfa. [4] Suka fito da dukan rundunansu da keken
yaƙi masu yawan gaske, babbar runduna, yawansu ya yi kamar yashin bakin teku.
[5] Duk sarakunan nan suka haɗa mayaƙansu tare, suka kafa sansani a bakin Ruwayen
Meron don su yi yaƙi da Isra’ilawa.
[6] UBANGIJI ya ce wa Yoshuwa, “Kada ka ji tsoronsu, domin war haka gobe zan ba da
dukansu a hannun Isra’ilawa, za su kuwa karkashe su. Za ku gurgunta dawakansu,
ku kuma ƙone keken yaƙinsu.”
[7] Sai Yoshuwa da dukan mayaƙan suka auka musu a bakin Ruwayen Meron.
[8] UBANGIJI kuwa ya ba Isra’ilawa nasara a kan su, suka ci su da yaƙi, suka fafare
su har zuwa Sidon Babba, zuwa Misrefot Mayim, har zuwa Kwarin Mizfa a gabas,
ba wanda suka bari da rai. [9] Yoshuwa ya yi musu yadda UBANGIJI ya umarta, ya
gurgunta dawakansu, ya kuma ƙone keken yaƙinsu.
[10] A lokacin nan Yoshuwa ya koma da baya ya ci Hazor da yaƙi, ya kuma kashe
sarkinta da takobi. (Hazor ce babbar masarautan ƙasashen nan.) [11] Suka karkashe
duk mazaunan ƙasar da takobi, ba su bar wani mai numfashi ba, suka kuma ƙona
Hazor.
[12] Yoshuwa ya ƙwace masarautun nan duka ya kuma kashe sarakunansu da takobi,
ya hallakar da su ƙaƙaf kamar yadda Musa bawan UBANGIJI ya umarta. [13] Duk da
haka Isra’ilawa ba su ƙone biranen da suke kan tuddai ba, sai Hazor kaɗai Yoshuwa
ya ƙone. [14] Isra’ilawa suka kwashi ganima da dabbobi na waɗannan birane, amma
suka karkashe mutanen duka da takobi, ba su bar wani mai numfashi ba. [15] Yadda
UBANGIJI ya umarci bawansa Musa, haka Musa ya umarci Yoshuwa, shi kuwa ya yi
duk abin da UBANGIJI ya umarci Musa.
[16] Saboda haka Yoshuwa ya cinye ƙasar duka da yaƙi, dukan Negeb, duka yankin
Goshen, filayen kwari na yamma, Araba da tuddai na Isra’ila da kwarinta. [17] Daga
Dutsen Halak wanda ya miƙe zuwa wajajen Seyir, zuwa Ba’al-Gad a Kwarin Lebanon
ƙasa da Dutsen Hermon. Ya kama sarakunansu ya karkashe su. [18] Yoshuwa ya daɗe
yana yaƙi da dukan waɗannan sarakuna. [19] Sai Hiwiyawa kaɗai waɗanda suke zama
a Gibeyon, sauran ba ko birni ɗaya da ta yi yarjejjeniya ta salama da Isra’ilawa,
Isra’ilawa kuwa suka ci dukansu da yaƙi. [20] Gama UBANGIJI ne ya taurare zukatansu

waɗannan sarakuna suka yi yaƙi da Isra'ilawa don yă hallaka su gaba ɗaya, yă gamar da su ba jinƙai, yadda UBANGIJI ya umarci Musa.

21 A lokacin nan Yoshuwa ya je ya hallaka Anakawa daga ƙasar tudu. Daga Hebron, Debir da Anab. Daga dukan ƙasar tuddai na Yahuda, da kuma dukan ƙasar tudu ta
Isra'ila, Yoshuwa ya hallaka su duka da garuruwansu. 22 Ba a bar waɗansu Anakawa
a harabar Isra'ila ba; sai dai a Gaza, Gat da Ashdod ne aka samu waɗanda suka ragu
da rai. 23 Yoshuwa kuwa ya ƙwace dukan ƙasar yadda UBANGIJI ya umarci Musa, ya
ba da ita ta zama ƙasar gādo ga Isra'ilawa, kabila-kabila.

Ta haka ƙasar ta huta daga yaƙi.

# 12

*Jerin sarakunan da aka ci da yaƙi*

1 Waɗannan su ne sarakunan ƙasashen da Isra'ilawa suka ci da yaƙi, suka kuma mallaki ƙasarsu a gabashin Urdun, daga kwarin Arnon zuwa Dutsen Hermon haɗe da dukan gefen gabas na Araba.

2 Sihon sarkin Amoriyawa, wanda ya yi mulki a Heshbon.

Ya yi mulki daga Arower wadda take iyakar kwarin Arnon, daga tsakiyar kwarin har zuwa, Kogin Yabbok, wanda yake iyakar Ammonawa. Wannan ya haɗa da rabin Gileyad.

3 Ya kuma yi mulki a kan gabashin Araba daga tekun Kinneret zuwa Tekun Araba (wato, Tekun Gishiri), zuwa Bet-Yeshimot da kuma kudu zuwa gangaren dutsen Fisga.

4 Haka ma suka ci sashen Og sarkin Bashan, ɗaya daga cikin Refahiyawa na ƙarshe da ya yi mulki a Ashtarot da Edireyi.

5 Mulkinsa ya taso daga Dutsen Hermon, da Saleka, da dukan Bashan har zuwa iyakar Geshurawa da Ma'akatiyawa haɗe da rabin Gileyad, zuwa kan iyakar Heshbon ta sarki Sihon.

6 Sai Musa, bawan UBANGIJI da Isra'ilawa suka ci Sihon da Og da yaƙi. Musa bawan UBANGIJI kuwa ya ba da ƙasarsu ga mutanen Ruben, mutanen Gad da kuma rabin mutanen kabilar Manasse.

7 Waɗannan su ne sarakuna da kuma ƙasashen da Yoshuwa da Isra'ilawa suka ci
da yaƙi a yammancin Urdun, daga Ba'al-Gad a Kwarin Lebanon zuwa Dutsen Halak
wanda ya miƙe zuwa Seyir. Yoshuwa ya raba ƙasarsu ta zama gādo ga Isra'ilawa
bisa ga yadda aka raba su kabila-kabila. 8 Kasar ta haɗa da ƙasar kan tudu, filayen
arewanci, Araba, gangaren Dutse, da jejin, da kuma Negeb, wato, ƙasashen Hittiyawa, Amoriyawa, Kan'aniyawa, Ferizziyawa, Hiwiyawa, da Yebusiyawa.

9 Sarkin Yeriko, ɗaya
sarkin Ai (kusa da Betel), ɗaya
10 sarkin Urushalima, ɗaya
sarkin Hebron, ɗaya
11 sarkin Yarmut, ɗaya
sarkin Lakish, ɗaya
12 sarkin Eglon, ɗaya
sarkin Gezer, ɗaya
13 sarkin Debir, ɗaya
sarkin Bet-Gader, ɗaya

14 sarkin Horma, ɗaya
sarkin Arad, ɗaya
15 sarkin Libna, ɗaya
sarkin Adullam, ɗaya
16 sarkin Makkeda, ɗaya
sarkin Betel, ɗaya
17 sarkin Taffuwa, ɗaya
sarkin Hefer, ɗaya
18 sarkin Afek, ɗaya
sarkin Sharon, ɗaya
19 sarkin Madon, ɗaya
sarkin Hazor, ɗaya
20 sarkin Shimron Meron, ɗaya
sarkin Akshaf, ɗaya
21 sarkin Ta'anak, ɗaya
sarkin Megiddo, ɗaya
22 sarkin Kedesh, ɗaya
sarkin Yokneyam a Karmel, ɗaya
23 sarkin Dor (A Nafot Dor), ɗaya
sarkin Goyim a Gilgal, ɗaya
24 sarki Tirza, ɗaya.

Duka-duka dai sarakuna talatin da ɗaya ne.

# 13

*Kasar da ba a riga an ƙwace ba tukuna*

1 Sa'ad da Yoshuwa ya tsufa, UBANGIJI ya ce masa, "Ka tsufa ƙwarai, ga shi kuma
akwai sauran ƙasa mai fāɗi da ba ku riga kun mallaka ba.

2 "Ga ƙasar da ta rage,

"dukan yankunan Filistiyawa da na Geshurawa. 3 Daga Kogin Shihor a gabashin Masar zuwa sashen Ekron a arewa, dukan wannan ƙasa ana lissafta ta a cikin ƙasar Kan'aniyawa, ko da yake tana a sashen da sarakuna biyar na Filistiyawa na Gaza, Ashdod, Ashkeloniyawa, Gat da Ekron;
na Awwiyawa. 4 Daga wajen kudu kuma,
dukan ƙasar Kan'aniyawa ce. Iyakarta a arewa ta fara daga Ara ta Sidoniyawa har zuwa Afek, ta zarce har zuwa iyakar Amoriyawa;
5 da ƙasar Gebaliyawa;
da dukan Lebanon wajen gabas daga Ba'al-Gad a gindin Dutsen Hermon zuwa Lebo Hamat.

6 "Dukan mazauna kan yankunan tuddai daga Lebanon zuwa Misrefot Mayim,
wato, dukan Sidoniyawa, ni da kaina zan kore su a gaban Isra'ilawa. Ka tabbata
ka raba wa Isra'ilawa ƙasar ta zama gādonsu kamar yadda na umarce ka, 7 ka raba
ta tă zama gādo wa kabilu tara da kuma rabin kabilar Manasse."

*Raba ƙasar da take gabashin Urdun*

8 Rabin kabilar Manasse, mutanen Ruben da mutanen Gad suka karɓi rabonsu na gādo wanda Musa ya ba su a gabashin Urdun. Abin da Musa bawan UBANGIJI ya ba su ke nan.

9 Wannan ya tashi daga Arower a gefen kwarin Arnon, da kuma daga garin da yake
tsakiyar kwarin, ya kuma haɗa da ƙasar da take tudun Medeba har zuwa Dibon,
10 da dukan garuruwan Sihon sarkin Amoriyawa, wanda ya yi mulkin Heshbon,
har zuwa iyakar Ammonawa.
11 Haɗe da Gileyad, inda mutanen Geshur da Ma'aka suke. Dukan Dutsen Hermon,
da dukan Bashan har zuwa Saleka, 12 wato, dukan masarautar Og a Bashan,
wanda ya yi mulkin Ashtarot da Edireyi, yana cikin waɗanda suke na ƙarshe
da ba a kashe ba a cikin Refahiyawa. Musa ya ci su da yaƙi, ya ƙwace ƙasarsu.
13 Amma Isra'ilawa ba su kori mutanen Geshur da Ma'aka ba, saboda haka suka
ci gaba da zama cikin Isra'ilawa har wa yau.

14 Kabilar Lawiyawa ne kaɗai Musa bai ba ta gādo ba, gama hadayun ƙonawa da
ake miƙa wa Ubangiji, Allah na Isra'ila ne gādonsu, kamar yadda ya yi musu
alkawari.

15 Ga abin da Musa ya ba kabilar Ruben bisa ga iyalansu.
16 Abin da ya kama daga Arower a gefen kwarin Arnon, da kuma daga garin da
yake tsakiyar kwarin, da dukan ƙasar tudu kusa da Medeba 17 zuwa Heshbon,
da dukan garuruwan kan tudu, haɗe da Dibon, Bamot Ba'al, Bet-Ba'al-Meyon,
18 Yahza, Kedemot, Mefa'at, 19 Kiriyatayim, Sibma, Zeret Shahar kan tudu cikin
kwari, 20 Bet-Feyor, gangaren Fisga da Bet-Yeshimot, 21 dukan garuruwan da suke
kan tudu da dukan masarautar Sihon sarkin Amoriyawa, wanda ya yi mulki a
Heshbon. Musa ya yi nasara da shi, da shugabannin Midiyawa, wato, Ewi, Rekem,
Zur, Hur, da Reba, sarakunan Sihon, waɗanda suka zauna a ƙasar. 22 Kari a kan
waɗanda aka kashe a yaƙi, Isra'ilawa suka kashe Bala'am ɗan Beyor da takobi
don yana duba.
23 Gefen Urdun shi ne iyakar mutanen Ruben. Waɗannan garuruwa da
ƙauyukansu su ne gādon mutanen Ruben, bisa ga iyalansu.

24 Ga abin da Musa ya ba kabilar Gad, bisa ga iyalansu.
25 Yankin ƙasarsu ya ƙunshi Yazer, da dukan garuruwan Gileyad, da rabin ƙasar
Ammonawa har zuwa Arower kusa da Rabba, 26 da kuma daga Heshbon zuwa
Ramat Mizfa da Betonim, da kuma daga Mahanayim zuwa sashen Debir, 27 kuma a
cikin kwari, Bet-Haram, Bet-Nimra, Sukkot da Zafon da kuma sauran masarautar
Sihon sarkin Heshbon (gabashin Urdun, abin da ya kama har zuwa ƙarshen
Tekun Kinneret).
28 Waɗannan garuruwan da ƙauyukansu duka, gādon mutanen Gad ne, bisa
ga iyalansu.

29 Ga abin da Musa ya ba rabin kabilar Manasse, wato, wa rabin zuriyar
Manasse, bisa ga iyalansu.
30 Abin da ya miƙe daga Mahanayim haɗe da dukan Bashan, da gefen masarautar
Og sarkin Bashan, da dukan garuruwan Yayir guda sittin da suke a Bashan, 31 da
rabin Gileyad, da Ashtarot, Edireyi (biranen sarki Og a Bashan).
Wannan shi ne rabon da zuriyar Makir ɗan Manasse suka samu, domin rabin
'ya'yan Makir maza, bisa ga iyalansu.

32 Waɗannan su ne rabon gādon da Musa ya yi lokacin da suke cikin filayen
Mowab a hayin gabashin Urdun kusa da Yeriko. 33 Amma Musa bai ba
kabilar Lawiyawa gādo ba; Ubangiji, Allah na Isra'ila, shi ne gādonsu
kamar yadda ya yi musu alkawari.

# 14

*Raba ƙasar yammancin Urdun*

1 Ga wuraren da Isra'ilawa suka sami gādo a ƙasar Kan'ana waɗanda Eleyazar
firist, Yoshuwa ɗan Nun da kuma shugabannin iyalai kabila-kabila na Isra'ila suka
raba musu. 2 Ta wurin yin ƙuri'a aka raba wa kabilan nan tara da rabi, yadda
UBANGIJI ya umarta ta wurin Musa. 3 Musa ya ba wa kabilan biyu da rabin nan
gādonsu gabashin Urdun, amma bai ba wa Lawiyawa gādo a cikin sauran ba, 4 gama
'ya'yan Yusuf sun zama kabilu biyu, Manasse da Efraim. Ba a ba Lawiyawa gādon
ba sai dai garuruwan da aka ba su su zauna a ciki, da wurin kiwo mai kyau domin
dabbobinsu. 5 Haka Isra'ilawa suka raba ƙasar, yadda UBANGIJI ya umarci Musa.

*An ba Kaleb Hebron*

6 Mutanen Yahuda kuma suka je wurin Yoshuwa a Gilgal, sai Kaleb ɗan Yefunne
Bakenizze ya ce wa Yoshuwa, "Ka san abin da UBANGIJI ya gaya wa Musa, mutumin
Allah a Kadesh Barneya game da kai da ni. 7 Ina da shekara arba'in lokacin da Musa
bawan UBANGIJI ya aike ni zuwa Kadesh Barneya in leƙi asirin ƙasar. Na kuwa kawo
masa rahoto daidai yadda na ga ƙasar, 8 amma 'yan'uwana waɗanda muka je tare
su suka ba da rahoton da ya sa zukatan mutane suka narke don tsoro. Ni kam na bi
UBANGIJI Allah da dukan zuciyata. 9 Saboda haka a ranan nan Musa ya rantse mini
cewa, 'Kasar da ka taka za tă zama ƙasarka ta gādo kai da 'ya'yanka har abada,
domin ka bi UBANGIJI Allahna da dukan zuciyarka.'

10 "Ga shi, kamar yadda UBANGIJI ya yi alkawari, ya bar ni da rai har na ƙara
shekaru arba'in da biyar tun daga lokacin da ya gaya wa Musa wannan, a lokacin da
Isra'ilawa suke yawo a cikin jeji. Ga ni nan yau shekaruna tamanin da biyar! 11 Ina
nan da ƙarfina kamar yadda nake da ƙarfi a lokacin da Musa ya aike ni; zan iya
fita zuwa yaƙi da ƙwazo yanzu kamar yadda nake zuwa a dā. 12 Yanzu sai ka ba ni
wannan ƙasar da take kan tudu wadda UBANGIJI ya yi alkawari zai ba ni a ranan nan.
Kai ma ka ji a lokacin, yadda Anakawa suke a can, biranensu manya ne kuma sun
kewaye su sosai, amma na sani UBANGIJI zai taimake ni, zan kore su kamar yadda ya
faɗa."

13 Sai Yoshuwa ya sa wa Kaleb ɗan Yefunne albarka, ya ba shi Hebron. 14 Saboda
haka Hebron ta zama ƙasar Kaleb ɗan Yefunne Bakenizze tun daga lokacin nan,
domin ya bi UBANGIJI, Allah na Isra'ila da dukan zuciyarsa. 15 (Dā a kan kira
wannan Hebron, Kiriyat Arba. Wannan Arba kuwa shi ne wani katon mutum a cikin
Anakawa.)

Sa'an nan ƙasar ta huta daga yaƙi.

# 15

*Rabo don kabilar Yahuda*

1 An raba wa kabilar Yahuda gādonsu ta wurin yin ƙuri'a, bisa ga iyalansu,
rabon ya kai har zuwa sashen Edom, zuwa Jejin Zin can kurewar kudu.

2 Iyakarsu a kudanci ta tashi tun daga kurewar kudu na Tekun Gishiri, 3 zuwa
kudancin Hanyar Kunama,* ta ci gaba har zuwa Zin, zuwa kudancin Kadesh
Barneya. Sa'an nan ta kurɗa zuwa Hezron har zuwa Addar, ta kuma karkata
zuwa Karka. 4 Sai ta wuce zuwa Azmon ta haɗu da Rafin Masar, ta ƙarasa a
Bahar Rum. Wannan shi ne iyakarsu ta kudu.

5 Iyakarsu ta gabas kuwa ita ce Tekun Gishiri wadda ta zarce har zuwa gaɓar Urdun.

* **15:3** Da Ibraniyanci Akrabbim

Iyakarsu ta arewa ta fara ne daga Tekun Gishiri a bakin Urdun, 6 wajen Bet-Hogla
ta wuce har zuwa arewancin Bet-Araba, zuwa Dutsen Bohan ɗan Ruben. 7 Sai
iyakar ta haura zuwa Debir daga Kwarin Akor ta juya arewa da Gilgal, wadda
take fuskantar hawan Adummim a kudancin kwari, ta ci gaba zuwa ruwan En
Shemesh, ta ɓullo ta En Rogel. 8 Sai kuma ta gangara zuwa Kwarin Ben Hinnom
a gangaren kudancin birnin Yebusiyawa (wato, Urushalima). Daga can ta haura
zuwa kan tudun a yammancin Kwarin Hinnom, a arewancin ƙarshen Kwarin
Refayim. 9 Daga kan tudun, iyakar ta nufi maɓulɓular ruwa na Neftowa, ta
ɓullo a garuruwan da suke a Dutsen Efron, ta gangara zuwa Ba'ala (wato, Kiriyat
Yeyarim). 10 Sa'an nan ta karkata yamma daga Ba'ala zuwa Dutsen Seyir, ta
wuce ta gangaren Dutsen Yeyarim (wato, Kesalon), ta ci gaba zuwa Bet-Shemesh,
ta bi zuwa Timna. 11 Ta wuce zuwa gangaren arewancin Ekron, ta juya zuwa
Shikkeron, ta wuce zuwa Dutsen Ba'ala, ta kai Yabneyel, iyakarta ta ƙare a teku.
12 Bakin Bahar Rum nan ne iyakar yammanci.

Wannan ita ce iyakar da ta kewaye jama'ar Yahuda bisa ga iyalansu.

*(Mahukunta 1.12-15)*

13 Yoshuwa ya ba Kaleb ɗan Yefunne wuri a Yahuda, Kiriyat Arba, wato, Hebron,
bisa ga umarnin UBANGIJI. (Arba shi ne mahaifin Anak.) 14 Daga can sai Kaleb ya kori
'ya'yan Anak, maza su uku daga Hebron, wato, Sheshai, Ahiman da Talmai. 15 Daga
can ya nufi Debir ya yi yaƙi da mutanen da suke zama a can (Dā sunan Debir, Kiriyat
Sefer ne). 16 Kaleb ya ce, "Zan ba da 'yata Aksa aure ga wanda zai ci Kiriyat Sefer
da yaƙi." 17 Otniyel ɗan Kenaz, ɗan'uwan Kaleb, ya ci Kiriyat Sefer da yaƙi; saboda
haka Kaleb ya ba wa Aksa 'yarsa, ya kuwa aure ta.

18 Wata rana da ta zo wurin Otniyel, sai ya zuga ta ta roƙi mahaifinta fili. Da ta
sauka daga kan jakinta sai Kaleb ya tambaye ta ya ce, "Me kike so in yi miki?"

19 Ta amsa ta ce, "Ka yi mini alheri na musamman, tun da ka ba ni wuri a Negeb,
ina roƙonka, ka ba ni maɓulɓulan ruwa." Kaleb kuwa ya ba ta maɓulɓulan ruwa na
tuddai da na kwari.

20 Wannan shi ne gādon kabilar Yahuda bisa ga iyalansu.

21 Garuruwan kabilar Yahuda da suke kudu cikin Negeb zuwa iyakar Edom su ne.
Kabzeyel, Eder, Yagur, 22 Kina, Dimona, Adada, 23 Kedesh, Hazor, Itnan, 24 Zif,
Telem, Beyalot, 25 Hazor-Hadatta, Keriyot Hezron (wato, Hazor), 26 Amam,
Shema, Molada, 27 Hazar Gadda, Heshmon, Bet-Felet, 28 Hazar Shuwal,
Beyersheba, Biziyotiya, 29 Ba'ala, Iyim, Ezem, 30 Eltolad, Kesil, Horma, 31 Ziklag,
Madmanna, Sansanna, 32 Lebayot, Shilhim, Ayin, Rimmon, jimillarsu, garuruwa
da ƙauyukansu duka ashirin da tara ne.
33 Biranen da suke a filayen kwari su ne,
Eshtawol, Zora; Ashna, 34 Zanowa, En Gannim, Taffuwa, Enam, 35 Yarmut,
Adullam, Soko, Azeka, 36 Sha'arayim, Aditayim, Gedera (Gederotayim ke nan).
Garuruwa goma sha huɗu ke nan da ƙauyukansu.
37 Zenan, Hadasha, Migdal Gad, 38 Dileyan, Mizfa, Yokteyel, 39 Lakish, Bozkat,
Eglon, 40 Kabbon, Lahman, Kitlish, 41 Gederot, Bet-Dagon, Na'ama, Makkeda,
garuruwa goma sha shida ke nan da ƙauyukansu.
42 Libna, Eter, Ashan, 43 Yefta, Ashna, Nezib, 44 Keyila, Akzib, Maresha, garuruwa
tara ke nan da ƙauyukansu.
45 Ekron da ƙauyukan da suke kewaye da ita; 46 yammancin Ekron da dukan
garuruwa da ƙauyukan da suke kusa da Ashdod. 47 Ashdod da garuruwa da

kuma ƙauyukan da suke kewaye da ita, Gaza da garuruwanta da ƙauyukanta har zuwa Rafin Masar da kuma Bahar Rum.
48 Birane na cikin ƙasar tuddai kuwa, su ne,
Shamir, Yattir, Soko, 49 Danna, Kiriyat Sanna (wato, Debir), 50 Anab, Eshtemo,
Anim, 51 Goshen, Holon, Gilo, garuruwa goma sha ɗaya ke nan da ƙauyukansu.
52 Arab, Duma, Eshan, 53 Yanum, Bet-Taffuwa, Afeka, 54 Humta, Kiriyat Arba
(wato, Hebron) da Ziyor, garuruwa tara ke nan da ƙauyukansu.
55 Mawon, Karmel, Zif, Yutta 56 Yezireyel, Yokdeyam, Zanowa, 57 Kayin, Gibeya,
Timna, garuruwa goma ke nan da ƙauyukansu.
58 Halhul, Bet-Zur, Gedor, 59 Ma'arat, Bet-Anot, Eltekon, garuruwa shida ke nan
da ƙauyukansu.
60 Kiriyat Ba'al (wato, Kiriyat Yeyarim) da Rabba, garuruwa biyu ke nan da ƙauyukansu.
61 Biranen da suke a jeji kuwa su ne,
Bet-Araba, Middin, Sekaka, 62 Nibshan, Birnin gishiri da En Gedi, garuruwa shida
ke nan da ƙauyukansu.

63 Kabilar Yahuda kuwa ba su iya korar Yebusiyawa waɗanda suke zama cikin Urushalima ba; har wa yau Yebusiyawa suna nan zaune tare da mutanen Yahuda.

# 16

*An raba wa Efraim da Manasse ƙasa ta wurin ƙuri'a*

1 Rabon da aka ba wa Yusuf ya fara tun daga Urdun kusa da Yeriko, gabas da ruwan
Yeriko, sai ya miƙe zuwa jeji, ya haura har zuwa cikin ƙasar tudu na Betel. 2 Ya
ci gaba daga Betel (wato, Luz), ya zarce zuwa sashen Arkitawa na Atarot, 3 ya
sauka zuwa yammancin bakin iyakar Yalfetiyawa har zuwa yankin Bet-Horon wanda yake cikin kwari. Ya zarce kuma zuwa Gezer, ya gangara ya yi ƙarshe a Bahar Rum.

4 Wannan ne yankin da aka ba wa Manasse da Efraim zuriyar Yusuf gādonsu.

5 Yankin Efraim ke nan bisa ga iyalansu.

Iyakar ƙasarsu ta gādo ta kama daga Atarot Addar a gabas zuwa Bet-Horon, 6 ta
wuce zuwa Bahar Rum. Daga Mikmetat a arewa kuwa iyakar ta karkata gabas
zuwa Ta'anat Shilo, ta wuce zuwa Yanowa a gabas. 7 Sai ta gangara daga Yanowa
zuwa Atarot da Na'ara, ta bi ta Yeriko, ta kuma fito ta Urdun. 8 Daga Taffuwa
kuma iyakar ta bi yamma zuwa kwazazzaban Kana, ta ƙarasa a Bahar Rum. Wannan shi ne gādon mutanen Efraim bisa ga iyalansu.
9 Gādon ya kuma haɗa da dukan garuruwa da ƙauyuka waɗanda aka keɓe wa mutanen Efraim daga cikin gādon mutanen Manasse.

10 Ba su kori Kan'aniyawan da suke zama a Gezer ba, don haka Kan'aniyawa suna zama tare da mutanen Efraim har wa yau; amma Kan'aniyawa suka zama masu yin aikin dole.

# 17

1 Wannan shi ne gādon da aka ba wa kabilar Manasse, a matsayin ɗan farin Yusuf. Manasse yana da ɗan farin mai suna Makir. Makir shi ne mahaifin mutanen Gileyad, aka ba shi Gileyad da Bashan gama Makiriyawa jarumai ne ƙwarai. 2 Aka kuma raba

wa sauran mutanen kabilar Manasse rabon gādonsu bisa ga iyalansu, wato, Abiyezer,
Helek, Asriyel, Shekem, Hefer da Shemida. Waɗannan su ne ʼyaʼyan Manasse, maza,
ɗan Yusuf bisa ga iyalansu.

3 Zelofehad kuwa ɗan Hefer, ɗan Gileyad, ɗan Makir, ɗan Manasse ba shi da ʼyaʼya
maza, sai dai mata. Ga sunayensu, Mala, Nowa, Hogla, Milka da Tirza. 4 Suka je
wurin Eleyazar firist, da Yoshuwa ɗan Nun, da kuma shugabannin, suka ce musu,
"UBANGIJI ya umarci Musa cewa yă ba mu gādonmu tare da ʼyanʼuwanmu maza."
Saboda haka Yoshuwa ya ba su gādo tare da ʼyanʼuwan mahaifinsu maza bisa ga
umarnin UBANGIJI. 5 Dalilin ke nan Manasse ya sami kashi goma ban da ƙasar Gileyad
da Bashan a gabashin Urdun, 6 domin ʼyaʼya mata na kabilar Manasse sun sami gādo
tare da ʼyaʼya maza. Aka ba wa sauran mutanen kabilar Manasse ƙasar Gileyad.

7 Iyakar ƙasar Manasse ta tashi daga Asher zuwa Mikmetat a gabashin Shekem.
Iyakar kuma ta miƙe har zuwa kudu wadda ta ƙunshi mutanen da suke zaune a
En Taffuwa. 8 (Manasse ne yake da ƙasar Taffuwa, amma garin Taffuwa kansa,
a kan iyakar Manasse ta mutanen Efraim ce.) 9 Saʼan nan iyakar ta ci gaba ta yi
kudu zuwa Rafin Kana. Akwai garuruwan da suke kudancin rafin, waɗanda suke
Efraim, ko da yake suna cikin yankin Manasse. Iyakar Manasse ta miƙe zuwa
arewa ta bi gefen rafin ta kuma ƙarasa a Bahar Rum. 10 Kasar a wajen kudu
ta Efraim ce, ta wajen arewa kuma ta Manasse ce. Bahar Rum ita ce iyakarsu.
Asher yana wajen arewa, Issakar kuma a wajen gabas.

11 A yanki tsakanin Issakar da Asher, Manasse yana da waɗannan wurare,
Bet-Sheyan, Ibileyam da ƙauyukanta, da mazaunan Dor da ƙauyukanta, da
mazaunan En Dor da ƙauyukanta, da mazaunan Taʼanak da ƙauyukanta, da
mazaunan Megiddo da ƙauyukanta (Na uku cikin jerin shi ne Nafot).

12 Duk da haka mutanen Manasse ba su iya mallakar garuruwan nan ba, domin
Kanʼaniyawa sun nace da zama a wannan yanki. 13 Da Israʼilawa suka yi ƙarfi, sai
suka sa Kanʼaniyawa suka zama masu yin musu aiki, amma ba su iya korarsu duka
ba.

14 Mutanen Yusuf kuwa suka ce wa Yoshuwa, "Me ya sa ka ba mu rabon gādo ɗaya
kawai? Ga shi muna da yawa kuma UBANGIJI ya albarkace mu sosai."

15 Yoshuwa ya ce musu, "In kuna da yawa sosai, in kuma ƙasar kan tudu ta Efraim
ba ta ishe ku ba, sai ku je cikin jeji, ku nema wa kanku ƙasa a ƙasar Ferizziyawa da
Refahiyawa."

16 Mutanen Yusuf suka amsa suka ce, "Kasar kan tudu ba ta ishe mu ba, ga kuma
Kanʼaniyawan da suke zama a filin, da waɗanda suke Bet-Sheyan da ƙauyukanta, da
waɗanda suke Kwarin Yezireyel, duk suna da keken yaƙin ƙarfe."

17 Amma Yoshuwa ya ce wa mutanen Yusuf, wa Efraim da Manasse, "Kuna da yawa,
kuna kuma da ƙarfi sosai. Ba wuri ɗaya kaɗai za ku samu gādo ba, 18 amma har da
ƙasar kan tudu ma, ko da yake jeji ne, ku je ku gyara shi, duk yă zama naku. Ko da
yake Kanʼaniyawa suna da kekunan yaƙi na ƙarfe, suna kuma da ƙarfi, duk da haka
za ku kore su."

# 18

*An raba sauran ƙasar*

1 Israʼilawa duka suka taru a Shilo suka kafa tenti inda za su dinga taruwa. Yanzu
ƙasar tana ƙarƙashin mulkinsu, 2 amma akwai sauran kabilu bakwai na Israʼila
waɗanda ba su samu rabon gādonsu ba tukuna.

3 Saboda haka Yoshuwa ya ce wa Isra'ilawa, "Har yaushe za ku yi jinkirin shiga, ku
mallaki ƙasar da UBANGIJI Allah na iyayenku ya ba ku? 4 Ku ba da mutum uku daga
kowace kabila, ni kuwa in aike su, su zagaya dukan ƙasar su rubuta bayani game
da ita, bisa ga yadda za a raba ta gādo ga kowace kabila, sa'an nan su dawo wurina.
5 Za ku raba ƙasar kashi bakwai. Mutanen Yahuda za su ci gaba da kasancewa a
wurin da suke a kudu, sai kuma mutanen Yusuf a wurin da suke a arewa. 6 Bayan
kun auna ƙasar, ku raba ta kashi bakwai, sai ku kawo mini taswirar ƙasar. Ni kuma
in yi muku ƙuri'a a gaban UBANGIJI Allahnmu. 7 Lawiyawa ba su da rabo a cikinku,
domin aikin firistocin da suke yi wa UBANGIJI shi ne gādonsu. Gad, Ruben da rabin
kabilar Manasse kuwa sun riga sun samu gādonsu a gabashin gefen Urdun, Musa
bawan UBANGIJI ya ba su."

8 Da mutanen za su kama hanya su je su zāna yadda ƙasar take, Yoshuwa ya umarce
su cewa, "Ku je ku ga yadda ƙasar take. Sa'an nan ku dawo wurina, zan yi muku
ƙuri'a a nan Shilo a gaban UBANGIJI." 9 Mutanen kuwa suka tafi suka bi ta cikin
ƙasar, suka bayyana yadda take a rubuce, gari-gari, kashi bakwai, suka koma wurin
Yoshuwa a Shilo.

10 Sai Yoshuwa ya yi musu ƙuri'a a gaban UBANGIJI, a nan ne ya raba wa
Isra'ilawa ƙasar bisa ga yadda aka raba su kabila-kabila.

### *Rabon da kabilar Benyamin ta samu*

11 Kuri'ar kabilar Benyamin bisa ga iyalansu. Rabonsu ya kama daga ƙasar
da take tsakanin kabilar Yahuda da ta Yusuf.

12 Daga gefen arewa, iyakarsu ta kama ne daga Urdun, ta wuce arewa a gangaren
Yeriko, ta nufi yamma cikin ƙasar kan tudu, ta fito a jejin Bet-Awen. 13 Daga can
ta ƙetare zuwa gangaren Luz a kudu (wato, Betel), ta wuce zuwa Atarot Adda a
tudun arewa na kwarin Bet-Horon.

14 Daga tudun da yake fuskantar Bet-Horon a kudu, iyakar ta juya kudu ta gefen
yamma ta ɓullo a Kiriyat Ba'al (wato, Kiriyat Yeyarim), birnin Yahuda. Wannan
ita ce iyakar a wajen yamma.

15 A gefen kudu kuwa, iyakar ta fara daga ƙauyukan Kiriyat Yeyarim wajen yamma
sai ta miƙe zuwa maɓuɓɓugar ruwan Neftowa. 16 Iyakar ta gangara zuwa gefen
dutsen da yake fuskantar Kwarin Ben Hinnom, wanda yake arewa da Kwarin
Refayim. Ta ci gaba ta gangara ta Kwarin Hinnom ta yi kudu kusa da birnin
Yebusiyawa har zuwa En Rogel. 17 Sai ta nausa ta yi wajen arewa, zuwa En
Shemesh, ta ci gaba zuwa Gelilot, wanda yake fuskantar hawan Adummim. Daga
can ta gangara zuwa Dutsen Bohan, ɗan Ruben. 18 Sai ta wuce ta yi arewancin
gangaren Bet-Araba, ta wuce har zuwa cikin Araba. 19 Sa'an nan ta wuce zuwa
arewancin gangaren Bet-Hogla ta kuma ɓulla a arewancin gaɓar Tekun Gishiri,
a bakin Urdun a kudu. Wannan ita ce iyakar a wajen kudu.

20 Urdun shi ne iyaka a wajen gabas.

Waɗannan su ne iyakokin yankin ƙasar da iyalan kabilar Benyamin suka
gāda.

21 Waɗannan su ne garuruwan da kabilar Benyamin suke da su na gādo.

Yeriko, Bet-Hogla, Emek Keziz, 22 Bet-Araba, Zemarayim, Betel, 23 Awwim, Fara,
Ofra, 24 Kefar Ammoni, Ofni da Geba, garuruwa goma sha biyu ke nan da
ƙauyukansu.

25 Akwai kuma Gibeyon, Rama, Beyerot, 26 Mizfa Kefira, Moza, 27 Rekem, Irfeyel,
Tarala, 28 Zela, Hayelef, birnin Yebusiyawa (wato, Urushalima), Gibeya da Kiriyat,
garuruwa goma sha huɗu ke nan da ƙauyukansu.

Wannan shi ne rabon gādon kabilar Benyamin bisa ga iyalansu.

# 19

*Rabon don kabilar Simeyon*

[1] Kuri'a ta biyu ta fāɗa a kan kabilar Simeyon, bisa ga iyalansu. Kasarsu ta
gādo tana cikin yankin Yahuda. [2] Waɗannan su ne wuraren da suka gāda.
Beyersheba (ko Sheba), Molada, [3] Hazar Shuwal, Bilha, Ezem, [4] Eltolad, Betul,
Horma, [5] Ziklag, Bet-Markabot, Hazar-Susa, [6] Bet-Lebayot da Sharuhen, garuruwa
goma sha uku ke nan da ƙauyukansu.
[7] Akwai kuma Ayin, Rimmon, Eter da Ashan, garuruwa huɗu ke nan da
ƙauyukansu, [8] da kuma dukan ƙauyukan da suke kewaye da garuruwan nan
har zuwa Rama na Negeb (wato, Ba'alat-Beyer).

Wannan shi ne gādon kabilar Simeyon bisa ga iyalansu. [9] Daga cikin gādon
mutanen Yahuda ne aka fitar da gādon kabilar Simeyon, bisa ga iyalansu,
domin rabon da kabilar Yahuda suka samu ya fi ƙarfin abin da suke bukata.
Saboda haka kabilar gādon Simeyon yana cikin harabar Yahuda.

*Rabon da kabilar Zebulun ta samu*

[10] Kuri'a ta uku ta fāɗa a kan Zebulun bisa ga iyalansu.
Iyakar ƙasarsu ta gādo ta kai har Sarid. [11] Ta nufi yamma zuwa Marala, ta taɓa
Dabbeshet, ta wuce zuwa rafin da yake kusa da Yokneyam. [12] Daga Sarid, ta juya
gabas zuwa harabar Kislot Tabor, ta kuma wuce zuwa Daberat har zuwa Yafiya.
[13] Sa'an nan ta ci gaba, ta yi gabas zuwa Gat-Hefer da Et Kazin; ta ɓulla a Rimmon,
ta juya zuwa Neya. [14] A can ne iyakar ta kewaya zuwa Hannaton, sa'an nan ta
ƙarasa a Kwarin Ifta El.
[15] Zebulun ta ƙunshi garuruwa goma sha biyu da ƙauyukansu. Garuruwan sun
haɗa da Kattat, Nahalal, Shimron, Idala da Betlehem.

[16] Garuruwan nan da ƙauyukansu su ne gādon da kabilar Zebulun ta samu,
bisa ga iyalansu.

*Rabon da kabilar Issakar ta samu*

[17] Kuri'a ta huɗu ta fāɗa a kan kabilar Issakar, bisa ga iyalansu. [18] Kasarsu
gādonsu ta haɗa da,
Yezireyel, Kessulot, Shunem, [19] Hafarayim, Anaharat, [20] Rabbat, Kishiyon, Ebez,
[21] Remet, En Gannim, En Hadda da Bet-Fazez.
[22] Iyakar ta taɓa Tabor Shahazuma da Bet-Shemesh ta kuma ƙarasa a Urdun.
Duka-duka garuruwa goma sha shida ke nan da ƙauyukansu.

[23] Waɗannan garuruwa da ƙauyukansu su ne rabon da kabilar Issakar ta
samu, bisa ga iyalansu.

*Rabon da kabilar Asher ta samu*

[24] Kuri'a ta biyar ta fāɗa a kan kabilar Asher, bisa ga iyalansu. [25] Kasarsu
gādonsu ta haɗa da,
Helkat, Hali, Beten, Akshaf, [26] Allammelek, Amad da Mishal. A arewanci kuma
iyakar ta taɓa Karmel da Shihor Libnat. [27] Sai ta yi gabas zuwa Bet-Dagon, ta
taɓa Zebulun da kuma Kwarin Ifta El, ta wuce arewa zuwa Bet-Emek da Neyiyel,
ta wuce Kabul a hagu, [28] ta kai Abdon, Rehob, Hammon da Kana, har zuwa Sidon
Babba. [29] Daga nan iyakar ta juya baya zuwa Rama, ta bi ta birnin nan mai
katanga na Taya, ta juya ta nufi Hosa, sa'an nan ta ɓulla ta Bahar Rum cikin
yankin Akzib, [30] Umma, Afek da Rehob.
Garuruwa ashirin da biyu ke nan da ƙauyukansu.

31 Garuruwan nan da ƙauyukansu su ne gādon da kabilar Asher ta samu bisa ga iyalansu.

*Rabon da kabilar Naftali ta samu*

32 Kuri'a ta shida ta fāɗa a kan kabilar Naftali, bisa ga iyalansu.
33 Iyakarsu ta kama daga Helef, daga babban itacen Mamre nan da yake a
Za'anannim, ta wuce Adami Nekeb da Yabneyel zuwa Lakkum, ta kuma ƙarasa
a Urdun. 34 Iyakar kuma ta juya yamma ta cikin Aznot-Tabo ta ɓulla a Hukkok.
Ta taɓa Zebulun a kudu, Asher a yamma, da kuma Urdun a gabas.
35 Biranen da suke da katanga su ne Ziddim, Zer, Hammat, Rakkat, Kinneret,
36 Adama, Rama, Hazor, 37 Kedesh, Edireyi, En Hazor, 38 Yiron, Migdal El, Horem,
Bet-Anat da Bet-Shemesh.
Garuruwa goma sha tara ke nan da ƙauyukansu.

39 Waɗannan garuruwa da ƙauyukansu su ne rabon da kabilar Naftali ta samu, bisa ga iyalansu.

*Rabon da kabilar Dan ta samu*

40 Kuri'a ta bakwai ta fāɗa a kan kabilar Dan, bisa ga iyalansu. 41 Kasarsu
ta gādo ta haɗa da,
Zora, Eshtawol, Ir Shemesh, 42 Shalim, Aiyalon, Itla, 43 Elon, Timna, Ekron, 44 Elteke,
Gibbeton, Ba'alat, 45 Yehud, Bene-Berak, Gat-Rimmon, 46 Me Yarkon da Rakkon
tare da sashen da yake fuskantar Yaffa.

47 (Amma ya zama wa mutanen kabilar Dan da wahala su mallaki ƙasar da aka ba su gādo, saboda haka sai suka nufi Leshem suka ci su da yaƙi, suka karkashe mutanen wurin, suka mallake ta, suka zauna a ciki. Suka kuma sa wa Leshem, sunan kakansu, wato, Dan.)

48 Waɗannan garuruwa da ƙauyukansu su ne gādon kabilar Dan, bisa ga iyalansu.

*Rabon da Yoshuwa ya samu*

49 Sa'ad da aka gama raba gādon ƙasar bisa ga ƙuri'a. Sai Isra'ilawa suka ba
Yoshuwa ɗan Nun nasa rabo a cikinsu, 50 yadda UBANGIJI ya umarta, suka ba shi
garin da ya ce a ba shi, Timnat Serad a ƙasar tudu ta Efraim. Ya kuma gina garin
ya zauna a can.

51 Waɗannan su ne rabe-raben gādon da Eleyazar firist, Yoshuwa ɗan Nun, da kuma shugabannin kabilan iyalan Isra'ila suka rarraba ta hanyar jefa ƙuri'a a Shilo a gaban UBANGIJI a ƙofar Tentin Sujada. Da haka suka yi suka gama rarraba ƙasar.

# 20

*Biranen mafaka*
*(Kidaya 35.9-15; Maimaitawar Shari'a 19.1-13)*

1 Sai UBANGIJI ya ce wa Yoshuwa, 2 "Ka gaya wa Isra'ilawa su keɓe waɗansu birane
su zama biranen mafaka kamar yadda na umarce ku ta wurin Musa, 3 domin idan
wani ya kashe wani bisa kuskure ba da niyyar yin kisankai ba, mutumin zai iya
gudu zuwa can yă fake don kada a kashe shi. 4 Lokacin da ya gudu zuwa ɗaya daga
cikin biranen nan, sai yă tsaya a ƙofar birnin yă gaya wa dattawan wannan birni
damuwarsa. Sa'an nan su karɓe shi su ba shi wurin zama a cikin birninsu. 5 In mai
neman yă kashe shi don ramako ya bi shi zuwa can, ba za su miƙa shi ba domin
ba da niyya ya kashe wani ba, kuma ba fushi ne ya sa ya yi kisan ba. 6 Zai zauna
a wannan birni har sai taron jama'a sun yi masa shari'a, kuma har sai lokacin da

babban firist wanda yake aiki a lokacin ya mutu, sa'an nan zai iya koma garinsa na dā."

7 Saboda haka suka keɓe Kedesh a Galili a ƙasar kan tudu ta Naftali, Shekem a ƙasar kan tudu ta Efraim, da Kiriyat Arba (wato, Hebron) a ƙasar kan tudu ta Yahuda.
8 A hayin Urdun, gabas da Yeriko, suka keɓe Bezer ta jeji a kan tudu a cikin yankin kabilar Ruben, Ramot cikin Gileyad a kabilar Gad, da Golan cikin Bashan a kabilar
Manasse. 9 In wani mutumin Isra'ila ko kuma wani baƙon da yake zama a cikinsu, ya yi kisankai cikin kuskure, zai iya gudu zuwa biranen da aka keɓe, ba za a bari mai neman ramako yă kashe shi kafin jama'a su yi masa shari'a ba.

# 21

*Garuruwa domin Lawiyawa*

1 To, a lokacin, sai shugabannin iyalan Lawiyawa suka je wurin Eleyazar firist,
Yoshuwa ɗan Nun da kuma shugabannin sauran iyalan kabilu na Isra'ila a 2 Shilo
cikin Kan'ana, suka ce musu, "UBANGIJI ya yi umarni ta wurin Musa cewa a ba mu garuruwan da za mu zauna a ciki, da wurin kiwo mai kyau don dabbobinmu."

3 Saboda haka kamar yadda UBANGIJI ya umarta, sai Isra'ilawa suka ba wa Lawiyawa waɗannan garuruwa da wuraren kiwo daga cikin gādonsu.

4 Kuri'a ta farko ta fāɗa a kan Kohatawa bisa ga iyalansu. Sai aka ba wa Lawiyawa waɗanda suke 'yan zuriyar Haruna, firist, garuruwa goma sha uku daga kabilan Yahuda, Simeyon da Benyamin.

5 Sauran Kohatawan kuma aka ba su garuruwa goma daga iyalan kabilar Efraim, Dan da kuma rabi kabilar Manasse.

6 Aka kuma ba wa zuriyar Gershon garuruwa goma sha uku daga iyalan kabilan Issakar, Asher, Naftali, da kuma rabin kabilar Manasse a Bashan.

7 Aka ba wa zuriyar Merari bisa ga iyalansu, garuruwa goma sha biyu daga kabilan Ruben, Gad da Zebulun.

8 Haka Isra'ilawa suka ba wa Lawiyawa waɗannan garuruwa da wuraren kiwo masu kyau, yadda UBANGIJI ya umarta ta wurin Musa.

9 Daga kabilan Yahuda da Simeyon ne aka ba su waɗannan garuruwan da aka
ambata, 10 (ga garuruwan da aka ba wa zuriyar Haruna waɗanda suke daga iyalan Kohatawa na Lawiyawa, domin ƙuri'a ta farko ta fāɗa a kansu),

11 an ba su, Kiriyat Arba (wato, Hebron), da wurin kiwon da yake kewaye da
ƙasar kan tudu ta Yahuda. (Arba shi ne kakan Anak.) 12 Amma sai aka ba
Kaleb ɗan Yefunne filayen da kuma ƙauyukan da suke kewaye da birnin, su
zama nasa. 13 Sai aka ba zuriyar Haruna firist, ƙasar Hebron (garin masu
neman mafaka don sun yi kisa), da Libna, 14 da Yattir, da Eshtemowa, 15 da
Holon, da Debir, 16 da Ayin, da Yutta, da kuma Bet-Shemesh, tare da wuraren kiwonsu, garuruwa tara ke nan daga kabilun nan biyu, Yahuda da Simeyon.

17 Daga kabilar Benyamin kuwa aka ba su,
Gibeyon, Geba, 18 Anatot da Almon, tare da wuraren kiwonsu, garuruwa huɗu ke nan.

19 Duka-duka garuruwan firistoci, zuriyar Haruna, su goma sha uku ne tare da wuraren kiwonsu.

20 Aka kuma ba wa sauran Kohatawa, iyalan Lawiyawa, garuruwa daga kabilar Efraim.

21 A ƙasar kan tudu ta Efraim, aka ba su,
Shekem (garin masu neman mafaka don sun yi kisa) da Gezer, 22 Kibzayim da
Bet-Horon, tare da wuraren kiwonsu, garuruwa huɗu ke nan.
23 Haka kuma daga kabilar Dan, aka ba su,
Elteke, Gibbeton, 24 Aiyalon da Gat-Rimmon, tare da wuraren kiwonsu, garuruwa
huɗu ke nan.
25 Daga rabin kabilar Manasse kuwa aka ba su,
Ta'anak da Gat-Rimmon, tare da wuraren kiwonsu, garuruwa biyu ke nan.
26 Dukan garuruwan nan goma tare da wuraren kiwonsu ne aka ba sauran iyalan Kohatawa.

27 Aka ba wa zuriyar Gershon, waɗanda suke Lawiyawa, rabo.
Daga rabin kabilar Manasse,
Golan a cikin Bashan (garin masu neman mafaka don sun yi kisa), da Be'eshtera, tare da wuraren kiwonsu, garuruwa biyu ke nan;
28 daga kabilar Issakar kuma aka ba su
Kishiyon, Daberat, 29 Yarmut da En Gannim, tare da wuraren kiwonsu, garuruwa
huɗu ke nan;
30 daga kabilar Asher kuwa aka ba su,
Mishal, Abdon, 31 Helkat da Rehob, tare da wuraren kiwonsu, garuruwa huɗu ke
nan;
32 daga kabilar Naftali kuma aka ba su,
Kedesh a cikin Galili (garin masu neman mafaka don sun yi kisa), Hammon-Dor da kuma Kartan, tare da wuraren kiwonsu, garuruwa uku ke nan.
33 Duka-duka, garuruwan iyalan Gershonawa goma sha uku ne, tare da wuraren kiwonsu.

34 Aka ba wa iyalan Merari (sauran Lawiyawa) garuruwa,
daga kabilar Zebulun,
wato, Yokneyam, Karta, 35 Dimna da kuma Nahalal, tare da wuraren kiwonsu,
garuruwa huɗu ke nan;
36 daga kabilar Ruben kuma aka ba su,
Bezer, Yahza, 37 Kedemot da kuma Mefa'at, tare da wuraren kiwonsu, garuruwa
huɗu ke nan;
38 daga kabilar Gad kuwa aka ba su,
Ramot Gileyad (garin masu neman mafaka don sun yi kisa), Mahanayim,
39 Heshbon da kuma Yazer, tare da wuraren kiwonsu, garuruwa huɗu ke nan.
40 Duka-duka garuruwan da aka ba iyalan mutanen Merari, waɗanda su ne sauran Lawiyawa, garuruwa goma sha biyu ne.

41 Jimillar birane da wurarensu na kiwon da aka ba Lawiyawa daga cikin
mallakar jama'ar Isra'ila guda arba'in da takwas ne. 42 Dukan garuruwan
nan kowannensu yana kewaye da wurin kiwo.

43 Ubangiji kuwa ya ba Isra'ilawa dukan ƙasar da ya yi wa kakanninsu alkawari,
suka kuwa mallake ta, suka zauna a cikinta. 44 Ubangiji ya ba su hutawa a kowane
gefe kamar yadda ya yi wa kakanninsu alkawari, ba ko ɗaya daga cikin abokan
gābansu da ya iya cinsu da yaƙi. 45 Ubangiji kuwa ya cika kowane alkawarin alherin
da ya yi wa mutanen Isra'ila.

# 22

*Kabilun gabas sun dawo gida*

1 Yoshuwa ya kira mutanen Ruben, mutanen Gad, da rabin kabilar Manasse 2 ya
ce musu, "Kun yi duk abin da Musa bawan UBANGIJI ya umarta, kun kuma yi mini
biyayya cikin dukan umarnan da na ba ku. 3 Dukan waɗannan yawan kwanaki, har
zuwa yau, ba ku yashe 'yan'uwanku Isra'ilawa ba, amma kuka kiyaye umarnin da
UBANGIJI Allahnku ya ba ku. 4 Yanzu da UBANGIJI Allahnku ya ba 'yan'uwanku hutu
kamar yadda ya yi alkawari, sai ku koma gidajenku a ƙasar da Musa bawan UBANGIJI
ya ba ku a Urdun. 5 Amma ku yi hankali, ku kiyaye umarnai da kuma dokokin da
Musa bawan UBANGIJI ya ba ku. Ku ƙaunaci UBANGIJI Allahnku, ku yi tafiya kan
hanyarsa, ku yi biyayya da umarnansa, ku riƙe shi sosai, ku bauta masa da dukan
zuciyarku da kuma dukan ranku."

6 Sai Yoshuwa ya sa musu albarka, ya sallame su, suka kuwa tafi gidajensu. 7 (Musa
ya riga ya ba rabin kabilar Manasse gādo a Bashan; sauran rabin kabilar kuma
Yoshuwa ya ba su gādo tare 'yan'uwansu a yammacin hayin Urdun.) Sa'ad da
Yoshuwa ya sallame su su tafi gida, ya sa musu albarka, 8 ya ce, "Ku koma gidajenku
tare da dukiya mai yawa, babban garken dabbobi, azurfa da zinariya, tagulla da
ƙarfe, da tufafi masu yawa sosai, sai ku raba ganimar da kuka samu daga abokan
gābanku, da 'yan'uwanku."

9 Saboda haka sai mutanen Ruben, mutanen Gad da kuma rabin mutanen kabilar
Manasse, suka bar Isra'ilawa a Shilo cikin Kan'ana don su koma Gileyad, ƙasarsu,
wadda suka samu bisa ga umarnin UBANGIJI ta wurin Musa.

10 Da suka kai Gelilot kusa da Urdun cikin ƙasar Kan'ana, sai mutanen Ruben,
mutanen Gad da kuma rabin mutanen kabilar Manasse suka gina bagade a can, a
Urdun. 11 Sa'ad da Isra'ilawa suka ji cewa sun gina bagade a iyakar Kan'ana, a
Gelilot kusa da Urdun wajen gefensu na Isra'ilawa, 12 sai dukan Isra'ilawa suka taru
a Shilo don su je su yaƙe su.

13 Saboda haka sai Isra'ilawa suka aiki Finehas ɗan Eleyazar, firist, zuwa ƙasar
Gileyad, wurin mutanen Ruben, mutanen Gad da kuma rabin mutanen kabilar
Manasse. 14 Suka aiki shugabanni guda goma su tafi tare da shi, ɗaya daga kowace
kabilar Isra'ila, kowannensu shugaba ne a iyalansa.

15 Sa'ad da suka je Gileyad, wurin mutanen Ruben, mutanen Gad da kuma rabin
mutanen kabilar Manasse, sai suka ce musu, 16 "Dukan jama'ar UBANGIJI sun ce yaya
za ku juya wa Allah na Isra'ila baya haka? Yaya za ku daina bin UBANGIJI ku gina wa
kanku bagade, ku yi masa tawaye yanzu? 17 Zunubin da Feyor ya yi bai ishe mu ba
ne? Ga shi, har yanzu ba mu gama tsarkakewa daga wannan zunubi ba, ko da yake
annoba ta auko wa mutanen UBANGIJI! 18 Yanzu za ku daina bin UBANGIJI ne?

"In kuka yi wa UBANGIJI tawaye yau, gobe zai yi fushi da dukan mutanen Isra'ila.
19 Idan ƙasar mallakarku ƙazantacciya ce, sai ku haye zuwa ƙasar UBANGIJI, inda
tabanakul yake, mu zauna tare. Amma kada ku yi wa UBANGIJI, ko kuma ku yi
mana tawaye ta wurin gina wa kanku bagade wanda ba na UBANGIJI Allahnmu ba.
20 Lokacin da Akan ɗan Zera ya yi rashin aminci game da kayan da aka keɓe, fushinsa
UBANGIJI bai auko a kan mutanen Isra'ila duka ba? Ai, ba shi kaɗai ya mutu don
zunubinsa ba."

21 Sai mutanen Ruben, mutanen Gad da kuma rabin mutanen kabilar Manasse
suka amsa wa shugabannin iyalan Isra'ila suka ce, 22 "Maɗaukaki, Allah, UBANGIJI!
Maɗaukaki, Allah, UBANGIJI ya sani! In mun yi wannan cikin tawaye ko rashin
biyayya ga UBANGIJI ne, kada ku bar mu da rai yau. 23 Idan mun bar bin UBANGIJI,
muka gina wa kanmu bagade don mu miƙa hadayun ƙonawa, ko kuwa hadayun gari,
ko kuwa hadayun salama, to, bari UBANGIJI kansa ya sāka mana.

24 “A’a! Mun yi haka ne don tsoro, kada nan gaba ’ya’yanku su ce wa ’ya’yanmu,
‘Me ya haɗa ku da UBANGIJI, Allah na Isra’ila? 25 UBANGIJI ya sa Urdun ya zama
iyaka tsakaninmu da ku, ku mutanen Ruben da mutanen Gad! Ba ku da rabo cikin
UBANGIJI.’ ’Ya’yanku za su iya sa ’ya’yanmu su daina tsoron UBANGIJI.
26 “Shi ya sa muka ce, ‘Bari mu yi shiri mu gina bagade, amma ba na ƙona hadayu
ko na sadaka ba.’ 27 Sai dai yă zama shaida tsakaninmu da ku, da kuma waɗanda za
su zo a baya, cewa za mu yi wa UBANGIJI sujada a wurinsa mai tsarki, za mu miƙa
hadayunmu na ƙonawa, hadayu na zumunta. Sa’an nan, nan gaba ’ya’yanku ba za
su ce wa ’ya’yanmu, ‘Ba ku da rabo a cikin UBANGIJI ba.’
28 “Muka kuma ce, ‘In har suka ce mana, ko ’ya’yanmu haka, sai mu amsa mu ce
ku dubi bagaden da yake daidai da na UBANGIJI wanda iyayenmu suka gina, ba don
ƙona hadayu da kuma yin sadaka ba, sai dai don yă zama shaida tsakaninmu da ku.’
29 “Allah ya sawwaƙa mana mu tayar wa UBANGIJI mu bar binsa, har mu gina
bagade don miƙa hadayu na ƙonawa, da na gari, da na sadaka, ban da bagaden
UBANGIJI Allahnmu wanda yake tsaye a gaban tabanakul.”
30 Da Finehas firist, da shugabannin mutanen, shugabannin iyalan Isra’ila, suka
ji abin da mutanen Ruben, mutanen Gad da kuma rabin mutanen kabilar Manasse
suka ce, sai suka ji daɗi. 31 Sai Finehas ɗan Eleyazar, firist, ya ce wa mutanen Ruben,
mutanen Gad da kuma rabin mutanen kabilar Manasse, “Yau mun san UBANGIJI yana
tare da mu, domin ba ku yi wa UBANGIJI rashin aminci cikin wannan abu ba. Yanzu
kun kuɓutar da Isra’ilawa daga hannun UBANGIJI.”
32 Sai Finehas ɗan Eleyazar, firist, da shugabannin suka koma Kan’ana daga
saduwa da mutanen Ruben da mutanen Gad a Gileyad, suka kai wa Isra’ilawa rahoto.
33 Isra’ilawa suka ji daɗin rahoton da suka ji, suka kuma yi wa Allah yabo. Ba su sāke
yin maganar zuwa yaƙi don su rushe ƙasar da mutanen Ruben da mutanen Gad suke
ciki ba.
34 Sai mutanen Ruben da mutanen Gad suka ba wa wannan bagaden sunan, Shaida
Tsakaninmu, cewa UBANGIJI Allah ne.

# 23

*Yoshuwa ya yi wa shugabanni bankwana*

1 An daɗe bayan da UBANGIJI ya ba Isra’ilawa hutu daga dukan abokan gāban
da suke kewaye da su. Yoshuwa kuwa ya tsufa, shekarunsa sun yi yawa, 2 sai
ya aika a kira Isra’ilawa duka, dattawansu, shugabanninsu, alƙalansu, da manyan
ma’aikatansu, ya ce musu, “Na tsufa, shekaruna kuwa sun yi yawa, 3 ku kanku kun
ga dukan abubuwan da UBANGIJI Allahnku ya yi da idanunku wa dukan ƙasashen
nan, UBANGIJI Allahnku shi ne wanda ya yi yaƙi dominku. 4 Ku tuna yadda na rarraba
wa kabilanku ƙasashen nan su zama naku na gādo, dukan ƙasashen da suka rage,
ƙasashen da na ci da yaƙi, tsakanin Urdun da Bahar Rum a yamma. 5 UBANGIJI
Allahnku kansa zai kore su a madadinku. Zai fafare su a gabanku, za ku kuwa mallaki
ƙasarsu, yadda UBANGIJI Allah ya yi muku alkawari.
6 “Ku yi ƙarfin hali, ku yi hankali, ku yi biyayya da dukan abin da aka rubuta a
cikin Littafin Dokoki na Musa, ba tare da kun juya hagu ko dama ba. 7 Kada ku haɗa
kai da mutanen nan da suke zama cikinku; ba ruwanku da sunayen allolinsu, kada
ku rantse da su. Kada kuwa ku bauta musu ko kuwa ku rusuna musu. 8 Sai dai ku
riƙe UBANGIJI Allahnku da kyau, yadda kuka yi har zuwa yanzu.
9 “UBANGIJI ya kori manyan ƙasashe masu ƙarfi; har wa yau ba wanda ya iya cin
ku da yaƙi. 10 Mutum ɗaya a cikinku ya isa yă sa mutane dubu nasu su gudu, domin
UBANGIJI Allahnku yana yaƙi dominku, kamar yadda ya yi alkawari. 11 Saboda haka
sai ku kula da kanku sosai, ku ƙaunaci UBANGIJI Allahnku.

[12] “Amma in kuka juya baya kuka zama abokai ga waɗanda suka ragu suke zama
a cikinku a ƙasashen nan, har kuka yi auratayya da su, kuka haɗa kai da su, [13] ku
tabbata cewa UBANGIJI Allahnku ba zai kore muku mutanen ƙasashen nan ba, sai ma
su zama muku dutsen tuntuɓe da tarko, za su zama bulala a bayanku, ƙayayyuwa a
idanunku, har sai kun hallaka daga wannan ƙasa mai kyau wadda UBANGIJI Allahnku
ya ba ku.
[14] “Yanzu na kusa barin fuskar duniyan nan. Kun sani da dukan zuciyarku, da
dukan ranku cewa, Ba ko ɗaya daga cikin alkawuran da UBANGIJI Allahnku ya yi, da
bai cika ba. Kowane alkawari ya cika; ba ko ɗaya da bai cika ba. [15] Kamar yadda
UBANGIJI Allahnku kuwa ya cika kowane alkawari mai kyau, haka ma ba zai fasa
kawo muku bala’in da ya faɗi ba, sai ya hallaka ku daga wannan ƙasa mai kyau da
ya ba ku. [16] In kuka karya alkawarin UBANGIJI Allahnku wanda ya umarce ku, in
kuka je kuka bauta wa waɗansu alloli, kuka rusuna musu, fushin UBANGIJI zai sauko
a kanku, za ku kuwa hallaka da sauri daga ƙasan nan mai kyau da ya ba ku.”

# 24

*Sabunta alkawari a Shekem*

[1] Yoshuwa ya tattara dukan kabilan Isra’ila a Shekem. Ya aika a kira dattawa,
shugabanni, alƙalai da manyan ma’aikatan Isra’ila, suka kai kansu gaban Allah.
[2] Yoshuwa ya ce wa dukan mutanen, “Ga abin da UBANGIJI, Allah na Isra’ila ya
ce, ‘Dā can, kakanninku, Tera mahaifin Ibrahim, da Nahor sun zauna a hayin Kogin
Yuferites suka yi wa waɗansu alloli sujada. [3] Amma na ɗauki mahaifinku Ibrahim,
daga ƙasar da take can a hayin Kogin Yuferites, na kawo shi ƙasar Kan’ana, na kuma
ba shi ’ya’ya masu yawa. Na ba shi Ishaku, [4] ga Ishaku kuwa na ba shi Yaƙub da
Isuwa. Na ba Isuwa ƙasar kan tudu ta Seyir, amma Yaƙub da ’ya’yansa maza suka
gangara zuwa Masar.
[5] “ ‘Sai na aiki Musa da Haruna, na aukar wa Masarawa annobai, ta wurin abin
da na yi ne na fitar da ku. [6] Lokacin da na fitar da iyayenku daga Masar, suka zo
teku, sai Masarawa suka fafare su da kekunan yaƙi da dawakai har zuwa Jan Teku.
[7] Amma suka yi kuka ga UBANGIJI don taimako, ya kuwa sa duhu ya raba tsakaninsu
da Masarawa; ya sa teku ya rufe Masarawa. Kun gani da idanunku abin da na yi wa
Masarawa, sa’an nan kuka zauna a jeji na tsawon lokaci.
[8] “ ‘Na kawo ku ƙasar Amoriyawa waɗanda suke gabas da Urdun. Suka yi yaƙi da
ku, amma na ba da su a hannunku, na hallaka su a gabanku, kuka kuma mallaki
ƙasarsu. [9] Lokacin da Balak ɗan Ziffor, sarkin Mowab, ya yi shiri yă yaƙi Isra’ila, ya
aiki Bala’am ɗan Beyor don yă la’anta ku. [10] Amma ban saurari Bala’am ba, saboda
haka sai ya ma sa muku albarka, na kuɓutar da ku daga hannunsa.
[11] “ ‘Sai kuka ƙetare Urdun kuka isa Yeriko. Mutanen Yeriko suka yi faɗa da
ku, kamar yadda Amoriyawa, Ferizziyawa, Kan’aniyawa, Hittiyawa, Girgashiyawa,
Hiwiyawa, da Yebusiyawa suka yi, amma na ba da su a hannunku. [12] Na aika rina
ta kore su a idonku, haka kuma sarakunan Amoriyawan nan. Ba da takobinku ko
bakanku ne kuka yi haka ba. [13] Na ba ku ƙasar da ba ku yi wata wahala kafin ku
samu ba, na ba ku kuma biranen da ba ku gina ba; kuka kuma zauna a cikinsu, kuka
ci daga ’ya’yan itacensu da ’ya’yan zaitun da ba ku ne kuka shuka ba.’
[14] “Yanzu, sai ku ji tsoron UBANGIJI, ku bauta masa da dukan aminci. Ku zubar da
allolin da kakanninku suka yi musu sujada a hayin Kogin Yuferites da kuma a Masar,
ku bauta wa UBANGIJI. [15] Amma in kuka ga ba za ku iya bauta wa UBANGIJI ba, sai
ku zaɓa yau wanda za ku bauta masa, ko allolin da kakanninku suka bauta musu
a hayin Kogin Yuferites, ko kuma allolin Amoriyawa, waɗanda kuke zama a cikin
ƙasarsu. Amma da ni da gidana, UBANGIJI ne za mu bauta wa.”

16 Sai mutanen suka amsa suka ce, “Allah ya kiyashe mu da rabuwa da UBANGIJI
Allahnmu, har a ce mu bauta wa waɗansu alloli! 17 UBANGIJI Allahnmu ne da kansa
ya fitar da iyayenmu daga Masar, daga ƙasar bauta, ya yi manyan abubuwan al’ajabi,
a idanunmu. Ya kiyaye mu cikin dukan hanyar da muka bi, da cikin ƙasashen da
muka ratsa; 18 UBANGIJI kuwa ya kore mana dukan Amoriyawa, waɗanda suke zaune
a ƙasar. Don haka mu ma za mu bauta wa UBANGIJI, gama shi ne Allahnmu.”
19 Yoshuwa ya ce wa mutanen, “Ba za ku iya bauta wa UBANGIJI ba gama shi Allah
mai tsarki ne; mai kishi kuma. Ba zai gafarta muku zunubin tawaye ba. 20 In kuka
juya wa UBANGIJI baya, kuka bauta wa waɗansu alloli, zai juya yă kawo muku bala’i,
yă hallaka ku, yă kawo ƙarshenku.”
21 Amma mutanen suka ce wa Yoshuwa, “Mu dai! Za mu bauta wa UBANGIJI.”
22 Yoshuwa kuwa ya ce musu, “Ku ne shaidun kanku cewa kun zaɓi ku bauta wa
UBANGIJI.”
Suka amsa suka ce, “I, mu ne shaidun kanmu.”
23 Yoshuwa ya ce musu, “Yanzu sai ku zubar da allolin da suke cikinku, ku miƙa
wa UBANGIJI, Allah na Isra’ila zuciyarku.”
24 Mutanen kuma suka ce, “Za mu bauta wa UBANGIJI Allahnmu, mu kuma yi masa
biyayya.”
25 A wannan rana Yoshuwa ya yi alkawari saboda mutanen, kuma a can Shekem
ya tsara musu ƙa’idodi da dokoki. 26 Yoshuwa kuwa ya rubuta abubuwan nan a cikin
Littafin Dokoki na Allah. Sa’an nan ya ɗauki babban dutse ya ajiye a ƙarƙashin itacen
oak kusa da tsattsarkan wuri na UBANGIJI.
27 Ya ce wa duka mutanen, “Ku gani! Wannan dutse zai zama mana shaida, ya ji
duk maganar da UBANGIJI ya yi mana, zai zama muku shaida in ba ku yi wa Allahnku
gaskiya ba.”

### *An binne Yoshuwa a ƙasar alkawari*

28 Sai Yoshuwa ya sallami mutane, kowa ya tafi ƙasar da aka ba shi gādo.
29 Bayan waɗannan abubuwa, Yoshuwa ɗan Nun, bawan UBANGIJI, ya mutu yana
da shekaru ɗari da goma. 30 Suka kuma binne shi a ƙasarsa ta gādo, a Timnat Sera
a ƙasar kan tudu ta Efraim, arewa da Dutsen Ga’ash.
31 Isra’ilawa kuwa sun bauta wa UBANGIJI dukan kwanakin Yoshuwa, da kuma
kwanakin dattawan da ya bari, da waɗanda suka ga duk abin da UBANGIJI ya yi
wa Isra’ila.
32 Aka kuma binne ƙasusuwan Yusuf da aka kawo daga Masar, a Shekem a wurin
da Yaƙub ya saya da azurfa ɗari daga ’ya’yan Hamor, babban Shekem. Wurin ya
zama gādon zuriyar Yusuf.
33 Eleyazar ɗan Haruna, ya mutu aka binne shi a Gibeya, wurin da aka ba ɗansa
Finehas a ƙasar kan tudu ta Efraim.

# Mahukunta

*Isra'ila sun yaƙi sauran Kan'aniyawa*

1 Bayan da Yoshuwa ya rasu, Isra'ilawa suka tambayi UBANGIJI suka ce, "Wane ne
zai fara tafiya don yă yaƙi Kan'aniyawa dominmu?"
2 Sai UBANGIJI ya ce, "Yahuda zai tafi. Na riga na ba da ƙasar a hannunsu."
3 Sa'an nan mutane Yahuda suka ce wa mutanen Simeyon "Ku zo tare da mu a
yankin da aka ba mu rabon mu don mu yaƙi Kan'aniyawa. Mu ma mu bi ku wurin
naku." Saboda haka mutanen Simeyon suka tafi tare da su.
4 Sa'ad da Yahuda ya fāɗa musu, UBANGIJI kuwa ya ba da Kan'aniyawa da
Ferizziyawa a hannunsu, suka kuwa kashe mutum dubu goma a Bezek. 5 A can
suka iske Adoni-Bezek, suka yaƙe shi, suka fatattaki Kan'aniyawa da Ferizziyawa.
6 Sai Adoni-Bezek ya gudu, amma suka bi shi suka kama shi, suka yayyanka manyan
yatsotsinsa na hannu da na ƙafa.
7 Sa'an nan Adoni-Bezek ya ce, "Sarakuna saba'in waɗanda aka yayyanka manyan
yatsotsinsu na hannu da na ƙafa, sun yi kalan abinci a ƙarƙashin teburina. Ga shi
yanzu Allah ya rama abin da na yi musu." Suka zo da shi Urushalima, a can kuwa
ya mutu.
8 Mutanen Yahuda suka yaƙi Urushalima ita ma suka ci ta. Suka karkashe mutanen
birnin suka cinna mata wuta.
9 Bayan wannan, mutanen Yahuda suka gangara suka yaƙi Kan'aniyawan da suke
zaune a ƙasar tudu, Negeb, da gindin tuddai a yammanci. 10 Suka ci gaba suka yaƙi
Kan'aniyawan da suke zaune a Hebron (wadda dā ake kira Kiriyat Arba) suka kuma
ci Sheshai, Ahiman da Talmai da yaƙi.
11 Daga nan kuma suka ci gaba suka yaƙi mutanen da suke zaune a Debir (da ake
kira a dā Kiriyat Sefer).
12 Sai Kaleb ya ce, "Duk wanda ya fāɗa wa Kiriyat Sefer ya kuma ci ta da yaƙi,
zan ba shi 'yata Aksa yă aura." 13 Sai Otniyel ɗan Kenaz, ƙanen Kaleb ya ci birnin,
saboda haka Kaleb ya ba shi 'yarsa Aksa ya aura.
14 Wata rana da ta zo wurin Otniyel, sai ta zuga shi[*] yă roƙi mahaifinta fili. Sa'ad
da ta sauko daga jakinta, sai Kaleb ya ce mata, "Me zan yi miki?"
15 Sai ta ce, "Ka yi mini alheri na musamman. Da yake ka ba ni ƙasa a Negeb, to,
sai ka ba ni maɓulɓulan ruwa kuma." Sai Kaleb ya ba ta maɓulɓulan bisa da kuma
na ƙasa.
16 Zuriyar surukin Musa, Keniyawa, suka haura daga Birnin dabino[†] tare da
mutanen Yahuda don su zauna cikin mutanen Hamadan Yahuda a cikin Negeb kusa
da Arad.
17 Sa'an nan mutanen Yahuda suka tafi tare da 'yan'uwansu mutanen Simeyon
suka fāɗa wa Kan'aniyawan da suke zaune cikin Zefat, suka kuwa hallaka birnin
gaba ɗaya. Saboda haka aka kira wurin Horma.[‡] 18 Mutanen Yahuda kuma suka ci[§]
Gaza, Ashkelon, da Ekron, kowace birni tare da yankinsa.
19 UBANGIJI kuwa yana tare da mutane Yahuda. Suka mallaki ƙasar tudu, amma ba
su iya suka kori mutanen daga filaye ba, domin suna da keken yaƙin ƙarfe. 20 Yadda
Musa ya yi alkawari, sai aka ba Kaleb Hebron, wanda ya kori daga cikinta 'ya'ya
maza uku na Anak. 21 Ko da yake mutanen Benyamin sun kāsa su kori Yebusiyawa,

---

[*] **1:14** Da Ibraniyanci; Seftuwajin da Bulget Otniyel, ya zuga ta [†] **1:16** Wato, Yeriko [‡] **1:17** Horma yana nufin hallaka. [§] **1:18** Da Ibraniyanci; Seftuwajin Yahuda bai ci

waɗanda suke zaune a Urushalima; har yă zuwa yau, Yebusiyawa suna zaune a can
tare da mutanen Benyamin.
22 To, gidan Yusuf suka auka wa Betel, UBANGIJI kuwa yana tare da su. 23 Sa'ad da
suka aike mutane don su leƙi asirin Betel (da dā ake kira Luz), 24 'yan leƙen asirin
suka ga wani ya fito daga birnin sai suka ce masa, "Ka nuna mana yadda za mu shiga
birnin, mu kuwa za mu yi maka alheri." 25 Saboda haka ya nuna musu, suka kuwa
hallaka birnin, suka bar mutumin da dukan iyalinsa da rai. 26 Sa'an nan ya tafi ƙasar
Hittiyawa, inda ya gina birni ya kuma kira shi Luz, haka ake kira birnin har wa yau.
27 Amma Manasse ba su kori mutane Bet-Sheyan ko Ta'anak ko Dor ko Ibileyam ko
Megiddo tare da ƙauyukansu ba, gama Kan'aniyawa sun dāge su zauna a wannan
ƙasa. 28 Sa'ad da Isra'ila ta yi ƙarfi, sai suka tilasta Kan'aniyawa yin aikin gandu
amma ba su kore su gaba ɗaya ba. 29 Haka Efraim ma bai kori Kan'aniyawa da suke
zaune a Gezer ba, amma Kan'aniyawa suka ci gaba da zama tare da su. 30 Haka kuma
Zebulun bai kori Kan'aniyawa da suke zaune a Kitron da Nahalol, waɗanda suka
rage a cikinsu ba; sai dai sun sa su aikin gandu. 31 Haka Asher ma bai kori waɗanda
suke zama a Akko ko Sidon ko Ahlab ko Akzib ko Helba ko Afik ko kuma Rehob
ba, 32 kuma saboda wannan ne mutanen Asher suke zaune cikin mazaunan ƙasar
Kan'aniyawa. 33 Haka kuma Naftali bai kori waɗanda suke zaune a Bet-Shemesh ko
Bet-Anat; amma mutanen Naftali su ma suna zama a ciki Kan'aniyawa mazaunan
ƙasar, waɗanda suke zaune a Bet-Shemesh da Bet-Anat kuwa suka zama masu yi
musu aikin gandu. 34 Amoriyawa suka matsa wa mutanen Dan a ƙasar tudu, ba su
yarda musu su gangaro zuwa filaye ba. 35 Su Amoriyawa kuma suka dāge su zauna
a Dutsen-Heres, Aiyalon, da Sha'albim. Amma yayinda mutanen Yusuf suka ƙara
ƙarfi, sai suka su yin musu aikin gandu. 36 Iyakar Amoriyawa kuwa daga Mashigin
Kunama* zuwa Sela da kuma zuwa gaba.

# 2

*Mala'ikan UBANGIJI a Bokim*

1 Mala'ikan UBANGIJI ya haura daga Gilgal zuwa Bokim ya ce, "Na hauro da ku daga
Masar zuwa ƙasar da na rantse zan ba wa kakanninku. Na ce, 'Ba zan taɓa tā da
yarjejjeniyata da ku ba, 2 ku kuma kada ku shiga wata yarjejjeniya da mazaunan
ƙasan nan, sai dai za ku rurrushe bagadansu.' Duk da haka ba ku yi biyayya mini
ba. Me ya sa kuka yi haka? 3 Saboda haka ina gaya muku cewa ba zan kore su a
gabanku ba; za su zama muku ƙaya, gumakansu kuma za su zama muku tarko."
4 Da mala'ikan UBANGIJI ya faɗa wa dukan Isra'ilawa waɗannan abubuwa, sai
mutane suka yi kuka mai zafi, 5 sai suka sa wa wannan wuri suna, Bokim.* A nan
suka miƙa hadaya a gaban UBANGIJI.

*Rashin biyayya da shan kayi*

6 Bayan Yoshuwa ya sallami Isra'ilawa, sai suka tafi don su mallaki ƙasar, kowa da
nasa gādon. 7 Mutane suka bauta wa UBANGIJI duk tsawon kwanakin Yoshuwa da na
dattawan da suka rayu bayansa waɗanda suka ga manyan abubuwan da UBANGIJI ya
yi wa Isra'ila.
8 Yoshuwa ɗan Nun, bawan UBANGIJI, ya mutu yana da shekara ɗari da goma. 9 Aka
binne shi a ƙasar gādonsa, a Timnat Heres† a ƙasar tudu ta Efraim, arewa da Dutsen
Ga'ash.
10 Bayan tsaran nan duka suka rasu, sai wata tsara ta taso wadda ba tă san UBANGIJI
ko abin da ya yi wa Isra'ila ba. 11 Sai Isra'ilawa suka yi mugaye abubuwa a gaban

* **1:36** Da Ibraniyanci Akrabbim * **2:5** Bokim yana nufin masu kuka. † **2:9** An kuma santa kamar Timnat Sera (dubi Yosh 19.50 da Yosh 24.30).

UBANGIJI suka kuma bauta Ba’al. 12 Suka yashe UBANGIJI Allah na kakanninsu, wanda
ya fitar da su daga Masar. Suka bi suka kuma bauta alloli dabam-dabam na mutanen
da suke kewaye da su. Suka tsokani UBANGIJI ya yi fushi 13 domin sun bar shi suka
bauta wa Ba’al da Ashtarot. 14 Cikin fushinsa a kan Isra’ila UBANGIJI ya ba da su ga
hannun waɗanda suka kawo musu hari suka washe su. Ya sayar da su ga abokan
gābansu da suke kewaye da su, waɗanda ba za su iya yin tsayayya da su ba. 15 Duk
sa’ad da Isra’ila suka fita yaƙi, UBANGIJI yakan yi gāba da su don a ci su a yaƙi, kamar
dai yadda ya rantse musu. Suka kuwa shiga wahala ƙwarai.

16 Sa’an nan UBANGIJI ya naɗa mahukunta,‡ waɗanda suka cece su daga hannun
waɗannan musu hari. 17 Duk da haka ba su saurari mahukuntansu ba amma sai
suka shiga ha’inci da waɗansu alloli suka kuma bauta musu. Ba kamar kakanninsu
ba, nan da nan suka kauce daga hanyar da kakanninsu suka bi, hanyar biyayya
ga umarnan UBANGIJI. 18 Duk sa’ad da UBANGIJI ya naɗa musu mahukunci, yakan
kasance tare da mahukuncin, yă kuma cece su daga hannun abokan gāba, muddin
mahukuncin yana a raye; gama UBANGIJI yakan ji tausayinsu yayinda suke gunaguni
ƙarƙashin waɗanda suka danne su suke kuma gasa musu azaba. 19 Amma sa’ad
da mahukuncin ya mutu, mutanen suka koma hanyar da ta fi ta kakanninsu muni,
sukan bi waɗansu alloli suna bauta musu. Suka ƙi barin mugun ayyukansu da taurin
zuciyarsu.

20 Saboda haka sai UBANGIJI ya fusata da Isra’ila ya ce, “Domin wannan al’umma ta
tā da yarjejjeniyar da na yi da kakanninsu ba su kuwa saurare ni ba, 21 ba zan ƙara
kori wata al’ummar da Yoshuwa ya bari sa’ad da ya rasu ba. 22 Zan yi amfani da su
in gwada Isra’ila in ga ko za su bi hanyar UBANGIJI su kuma yi tafiya a cikinta kamar
yadda kakanninsu suka yi.” 23 UBANGIJI ya bar waɗannan al’ummai su kasance; bai
kore su nan take ta wurin ba da su a hannun Yoshuwa ba.

# 3

1 Waɗannan su ne al’umman da UBANGIJI ya bari don yă gwada duk waɗannan
Isra’ilawan da ba su san yaƙi a Kan’ana ba 2 (ya yi haka ne domin yă koya wa zuriyar
Isra’ilawa waɗanda ba su taɓa yin yaƙi a dā ba), 3 sarakuna biyar na Filistiyawa,
dukan Kan’aniyawa, Sidoniyawa, da kuma Hiwiyawan da suke zaune a duwatsun
Lebanon daga Dutsen Ba’al-Hermon zuwa Lebo* Hamat. 4 An bar su domin su gwada
Isra’ilawa a ga ko za su yi biyayya da umarnin UBANGIJI, wanda ya ba wa kakanninsu
ta wurin Musa.

5 Isra’ilawa suka zauna tare da Kan’aniyawa da Hittiyawa, Amoriyawa, Fer-
izziyawa, Hiwiyawa da kuma Yebusiyawa. 6 Suka auri ’ya’yansu mata, su ma suka
bar ’ya’yansu maza suka auri ’ya’yansu mata, suka kuma yi wa gumakansu sujada.

### *Otniyel*

7 Isra’ilawa suka aikata mugunta a gaban UBANGIJI; suka manta da UBANGIJI
Allahnsu suka kuma bauta wa Ba’al da Ashera. 8 Fushin UBANGIJI kuwa ya yi ƙuna
a kan Isra’ila har ya sayar da su ga Kushan-Rishatayim sarkin Aram-Naharayim,† a
wurinsa ne Isra’ilawa suka zama bayi shekara takwas. 9 Amma da suka yi kuka ga
UBANGIJI, sai ya tad musu da mai ceto, Otniyel ɗan Kenaz, ƙanen Kaleb wanda ya cece
su. 10 Ruhun UBANGIJI ya sauko masa, domin yă zama mahukuncin‡ Isra’ila yă kuma
je yaƙi. UBANGIJI ya bayar da Kushan-Rishatayim sarkin Aram a hannun Otniyel, ya
kuwa sha ƙarfinsa. 11 Saboda haka ƙasar ta zauna da lafiya shekara arba’in har sai
da Otniyel ɗan Kenaz ya rasu.

‡ **2:16** Ko kuwa shugabanni; daidai kamar a ayoyi 17-19. * **3:3** Ko kuwa zuwa mashigi zuwa † **3:8** Wato, Arewancin Mesofotamiya ‡ **3:10** Ko kuwa shugaba

### *Ehud*

12 Isra'ilawa suka sāke aikata mugayen ayyuka a gaban UBANGIJI, saboda sun aikata
wannan mugunta sai UBANGIJI ya ba wa Eglon sarkin Mowab ƙarfi a kan Isra'ila. 13 Da
ya sami Ammonawa da Amalekawa suka haɗa hannu tare, sai Eglon ya tafi ya auka
wa Isra'ila, suka ƙwace Birnin Dabino.§ 14 Isra'ilawa suka zama bayin Eglon sarkin
Mowab shekara goma sha takwas.

15 Isra'ilawa suka sāke yin kuka ga UBANGIJI, ya kuwa ba su mai ceto, Ehud, wani
bahago, ɗan Gera daga kabilar Benyamin. Isra'ilawa suka aike shi da haraji wurin
Eglon sarkin Mowab. 16 To, Ehud ya riga ya ƙera takobi mai kaifi biyu mai tsawo
wajen kamu ɗaya da rabi, wanda ya yi ɗamara da shi a cinyarsa ta dama ƙarƙashin
rigarsa. 17 Ya kai wa Eglon sarkin Mowab harajin, wanda yake mai ƙiba ne. 18 Bayan
Ehud ya ba da harajin, sai ya sallame mutanen da suka ɗauko harajin. 19 A wajen
gumaka* kusa da Gilgal, shi kansa ya juya ya koma ya ce, "Ranka yă daɗe, ina da
saƙo na asiri dominka."

Sarkin ya ce, "Ku ba mu wuri!" Sai dukan fadawansa suka fita.

20 Sai Ehud ya matso yayinda shi kuwa yake zaune shi kaɗai a ɗakin sama mai
sanyi a fadansa† ya ce, "Ina da saƙo daga wurin Allah dominka." Sarki ya tashi daga
kujerarsa, 21 Ehud ya kai hannun hagunsa, ya zaro takobi daga cinyar ƙafar damansa
ya soki sarki a ciki. 22 Har ƙotar ma ta shige ciki, takobin kuma ya fito ta bayansa.
Ehud bai zare takobin ba, kitse kuwa ya rufe shi. 23 Sa'an nan Ehud ya fita daga
shirayin;‡ ya rufe ƙofar ɗakin saman, ya kuma kulle su.

24 Bayan da ya tafi, bayin sarki suka zo suka tarar duk ƙofofin ɗakin sama suna
kulle, suka ce, "Wataƙila yana bayan gari ne a ɗakin ciki." 25 Suka yi ta jira har suka
gaji. Da suka ga dai bai buɗe ƙofar ba, sai suka ɗauki mabuɗi, suka buɗe. Sai ga
shugabansu a ƙasa matacce.

26 Yayinda suke fama jira, Ehud ya riga ya yi gaba. Ya bi ta wajen gumaka zuwa
Seyira. 27 Da ya iso can, sai ya busa ƙaho a ƙasar tudu ta Efraim, Isra'ilawa kuma
suka gangaro tare da shi daga tuddai, shi kuwa yana jagorarsu.

28 Ya umarce su ya ce, "Ku bi ni, gama UBANGIJI ya ba Mowab abokin gābanku a
hannunku." Haka suka gangaro tare da shi suna mallaki mashigin Urdun da ta shiga
zuwa Mowab, ba su yarda wani ya haye ba. 29 A lokacin sun kashe mutanen Mowab
dubu goma, dukansu jarumawa da masu ji da ƙarfi; ba ko ɗaya da ya tsira. 30 A
wannan rana aka mai da Mowab bayin Isra'ila, ƙasar kuwa ta sami zaman lafiya
shekara takwas.

### *Shamgar*

31 Bayan Ehud, sai Shamgar ɗan Anat, wanda ya karkashe Filistiyawa ɗari shida
da sandar korar shanun noma, shi ma ya ceci Isra'ila.

# 4

### *Debora*

1 Bayan rasuwar Ehud, Isra'ilawa suka sāke aikata mugayen ayyuka a gaban
UBANGIJI. 2 Saboda haka UBANGIJI ya sayar da su ga Yabin sarkin Kan'ana wanda yake
mulki a Hazor. Shugaban mayaƙansa shi ne Sisera, wanda yake zaune a Haroshet
Haggoyim. 3 Domin Yabin sarkin Kan'ana yana da kekunan yaƙin ƙarfe ɗari tara,
ya ji wa Isra'ilawa ƙwarai har shekara ashirin, sai suka yi kuka ga UBANGIJI, don
taimako.

---

§ **3:13** Wato, Yeriko * **3:19** Ko kuwa wurin fashe duwatsu; haka ma a aya 26. † **3:20** Ma'anar wannan magana a Ibraniyanci babu tabbas. ‡ **3:23** Ma'anar kalman nan a Ibraniyanci ba a tabbatar ba.

4 A lokacin Debora annabiya, matar Laffidot ce take bi* da Isra'ila. 5 Takan yi zaman
shari'a a ƙarƙashin Dabinon Debora tsakanin Rama da Betel, a ƙasar tudu ta Efraim,
Isra'ilawa kuwa sukan zo wurinta don tă yi musu shari'a. 6 Sai ta aika a kira mata
Barak ɗan Abinowam daga Kedesh a Naftali, ta ce masa, "UBANGIJI, Allah na Isra'ila
ya umarce ka, 'Je ka, ka ɗauki mutane Naftali da na Zebulun dubu goma tare da kai,
ka yi jagoransu zuwa Dutse Tabor. 7 Zan jawo Sisera, shugaban mayaƙan Yabin, da
keken yaƙinsa da mayaƙansa zuwa Kogin Kishon in ba da su a hannunku.' "

8 Barak ya ce, "In kika tafi tare da ni, zan tafi; amma in ba ki zo tare da ni ba, ba zan tafi ba."

9 Debora ta ce, "To, shi ke nan, zan tafi tare da kai. Amma saboda yadda ka ɗauki
wannan batun, darajar ba za tă zama taka ba, gama UBANGIJI zai ba da Sisera a
hannun mace." Saboda haka Debora ta tafi tare da Barak zuwa Kedesh, 10 a can
Barak ya kira Zebulun da Naftali. Mutum dubu goma suka kuma bi shi, Debora kuma tana tare da shi.

11 To, Heber Bakene ya riga ya bar Keniyawa, zuriyar Hobab, ɗan'uwan† matar Musa, ya kafa tentinsa wajen babban itace a Za'anannim kusa da Kedesh.

12 Sa'ad da aka gaya wa Sisera cewa Barak ɗan Abinowam ya haura zuwa dutsen
Tabor, 13 sai Sisera ya tattara keken yaƙinsa na ƙarfe ɗari tara wuri ɗaya da dukan mutanen da suke tare da shi daga Haroshet Haggoyim zuwa Kogin Kishon.

14 Sa'an nan Debora ta ce wa Barak, "Je ka! Wannan ita ce ranar da UBANGIJI ya ba da Sisera a hannunka. Ba UBANGIJI ya riga ya sha gabanka?" Saboda haka Barak
ya gangara zuwa Dutsen Tabor, da mutum dubu goma biye da shi. 15 Da matsowar
Barak, UBANGIJI ya murƙushe Sisera da dukan sarakunansa da mayaƙansa da takobi,
Sisera kuwa ya gudu da ƙafa ya bar keken yaƙinsa. 16 Amma Barak ya bi keken
yaƙin da mayaƙan har Haroshet Haggoyim. Aka karkashe dukan mayaƙan Sisera ba ko ɗayan da ya tsira.

17 Amma Sisera, ya tsere da ƙafa zuwa tentin Yayel, matar Heber Bakene, domin suna da abokantaka da Yabin sarkin Hazor da kuma kabilar Heber Bakene.

18 Yayel ta fito ta taryi Sisera ta ce masa, "Ranka yă daɗe, ka shigo, ka shigo ciki. Kada ka ji tsoro." Saboda haka ya shiga cikin tentinta, sai ta rufe shi da bargo.

19 Sai ya ce, "Ina roƙonki, ki ba ni ruwa in sha, ina jin ƙishirwa." Sai ta buɗe salkar madara, ta ba shi ya sha, sai ta kuma rufe shi.

20 Ya ce mata, "Ki tsaya a ƙofar tenti, in wani ya zo ya tambaye ki, 'Akwai wani a nan?' Ki ce masa 'a'a.' "

21 Amma Yayel, matar Heber, ta ɗauki turken tenti da guduma ta tafi wurinsa da sauri sa'ad da yake barci saboda gajiya. Ta kafa masa turken a gindin kunnensa ta haɗa shi da ƙasa, har ya mutu.

22 Sai ga Barak mai bin sawun Sisera, Yayel kuwa ta fito don marabtarsa, ta ce, "Shigo, zan nuna maka mutumin da kake nema." Saboda haka ya shiga ciki tare da ita, sai ga Sisera kwance da turken a gindin kunnensa, matacce.

23 A ranar Allah ya yi kaca-kaca da Yabin, sarkin Kan'ana a gaban Isra'ila.
24 Isra'ilawa kuwa suka ƙara ƙarfi gāba da Yabin, sarkin Kan'aniyawa, har suka hallaka shi.

# 5

*Waƙar Debora*

1 A wannan rana ce Debora da Barak ɗan Abinowam suka rera wannan waƙa.
2 "Sa'ad da 'ya'yan sarki a Isra'ila suka yi jagora,
sa'ad da mutane suka niyya su ba da kansu,
suna yabon UBANGIJI!

* 4:4 A al'adance mahukunta † 4:11 Ko kuwa baban

3 “Ya sarakuna, ku ji! Ku saurara, ku masu mulki!
Zan yi waƙa ga UBANGIJI, zan yi waƙa;
zan yi kaɗe-kaɗe ga UBANGIJI, Allah na Isra’ila.

4 “Ya UBANGIJI, sa’ad da ka bar Seyir,
sa’ad da ka yi tafiya daga ƙasar Edom,
ƙasa ta girgiza, sammai suka zubo,
gizagizai sun zubo da ruwa.
5 Duwatsu suka girgizu a gaban UBANGIJI, Wannan na Sinai,
a gaban UBANGIJI, Allah na Isra’ila.

6 “A zamanin Shamgar ɗan Anat,
a zamanin Yayel, an yashe dukan hanyoyi;
matafiye suka bi hanyoyin da suka yi kona-kona.
7 Rayuwar ƙauye* a Isra’ila ta daina,
ta daina sai da ni, Debora, na taso,
na taso mahaifiya a Isra’ila.
8 Sa’ad da suka zaɓi sababbin alloli,
sai ga yaƙi a ƙofofin birnin,
ba a kuwa ga garkuwa ko māshi
a cikin mutum dubu arba’in a Isra’ila ba.
9 Zuciyata tana tare da ’ya’yan sarakunan Isra’ila,
tare da masu niyyar ba da kansu da yardan rai cikin mutane.
Yabo ya tabbata ga UBANGIJI!

10 “Ku da kuke hawan fararen jakuna,
kuna zama a sirdin barguna,
da ku da kuke tafiya a kan hanya,
ku kula 11 da muryoyin mawaƙa a wuraren ruwaye.
Suna faɗi ayyukan adalcin UBANGIJI,
ayyukan adalcin mayaƙansa a Isra’ila.

“Sa’an nan mutanen UBANGIJI
suka gangara zuwa ƙofofin birni.
12 ‘Ki farka, ki farka, Debora!
Ki farka, ki farka, ki tā da waƙa!
Ka farka, ya Barak!
Ka ta sa kamammunka gaba, ya ɗan Abinowam.’

13 “Sa’an nan waɗanda aka bari
suka sauko zuwa wajen shugabanni;
mutane na UBANGIJI
suka zo wurina tare da masu ƙarfi.
14 Waɗansu suka zo daga Efraim, waɗanda ainihinsu daga Amalek ne;
Benyamin yana tare da mutanen da suka bi ka.
Daga Makir, shugabannin sojoji suka gangaro,
daga Zebulun waɗanda suke riƙe da sandan komanda suka fito.
15 ’Ya’yan sarautar Issakar suna tare da Debora;
I, Issakar yana tare da Barak,

* 5:7 Ko kuwa Jarumawa

yana binsa a guje zuwa kwari.
A yankunan Ruben
aka kuma bincike zuciya sosai.
16 Don me kuka tsaya a wutar sansani
don ku ji makiyaya suna kiran garkuna?
A yankunan Ruben
aka yi bincike zuciya sosai.
17 Gileyad ya tsaya gaban Urdun.
Kai kuma Dan, don me ka ka yi ta zama a wajen jiragen ruwa?
Asher ya ci gaba da kasance a bakin teku
ya kasance a wuraren zamansa.
18 Mutanen Zebulun sun kasai da rayukansu;
haka ma Naftali a bakin dāgā.

19 “Sarakuna suka zo, suka yi yaƙi;
sarakunan Kan’ana sun yi yaƙi
a Ta’anak a gefen ruwan Megiddo,
amma ba su ɗauki azurfa, ko ganima ba.
20 Daga sama taurari suka yi faɗa,
daga bakin tekuna suka yi yaƙi da Sisera.
21 Kogin Kishon ya kwashe su,
tsohon kogi, kogin Kishon.
Ci gaba raina; ka ƙarfafa!
22 Sa’an nan kofatan dawakai suka ƙwaƙula,
suna sukuwa, haka dawakansa masu ƙarfi suke tafiya.
23 Mala’ikan Ubangiji ya ce, ‘Ka la’anci Meroz.’
‘Ka la’anci mutanensa sosai,
domin ba su kawo wa Ubangiji taimako ba,
su kawo wa Ubangiji taimako a kan masu ƙarfi ba.’

24 “Mafi albarka a ciki mata ta zama Yayel
matar Heber Bakene,
mafi albarka na mata masu zama a alfarma.
25 Ya nemi ruwa, ta kuwa ta ba shi madara;
a ƙwaryar da ta dace da sarakuna ta kawo masa kindirmo.
26 Hannunta ya ɗauki turken tenti,
da hannunta na dama ta ɗauko guduma.
Ta bugi Sisera, ta ragargaza kansa,
ta ragargaza ta huda kunnensa.
27 A ƙafafunta ya fāɗi,
ya fāɗi; a can ya kwanta.
A ƙafafunta ya fāɗi, ya fāɗi;
a can ya fāɗi, matacce.

28 “Ta taga mahaifiyar Sisera ta leƙa;
a bayan madogarar ƙofa ta yi ta ihu,
‘Me ya sa keken yaƙinsa ta daɗe ba tă dawo ba?
Me ya sa dawakan keken yaƙinsa ba su dawo da wuri ba?’
29 Mafi hikima cikin ’yan matanta suka amsa mata,
tabbatacce, ta ci gaba ta ce wa kanta,

30 ‘Ba nema suke su raba ganima ba,
yarinya guda ko biyu wa kowane mutum,
riguna masu launi a matsayin ganima don Sisera,
riguna masu ado,
riguna masu ado sosai don wuyata,
dukan wannan a matsayin ganima?’

31 “Ta haka bari dukan abokan gābanka su hallaka, ya Ubangiji!
Amma bari waɗanda suke ƙaunarka su zama kamar rana
sa’ad da ta fito da ƙarfinta.”
Sa’an nan ƙasar ta sami zaman lafiya shekara arba’in.

# 6

### *Gideyon*

1 Isra’ilawa suka sāke yin mugayen ayyuka a gaban Ubangiji, sai ya ba da su ga
Midiyawa shekara bakwai. 2 Da Midiyawa suka matsa musu sosai, sai Isra’ilawa suka
yi wa kansu mafakai a rammukan duwatsu, kogona da kuma mafaka. 3 Duk lokacin
da Isra’ilawa suka yi shuka sai Midiyawa da Amalekawa da waɗansu mutane daga
gabashi sukan kai musu hari. 4 Sukan yi sansani a ƙasar sun lalatar da hatsi har
zuwa Gaza kuma ba sa barin wani abu mai rai wa Isra’ila, ko tumaki ko shanu ko
jakuna. 5 Sukan zo da dabbobinsu da tentinsu kamar tarin fāri. Yana da wuya a
ƙidaya yawan mutanen da kuma raƙumansu; sukan mamaye ƙasar don su lalatar
da ita. 6 Midiyawa suka talauce Isra’ilawa ƙwarai, har ya sa suka yi kuka ga Ubangiji
don taimako.
7 Sa’ad da Isra’ilawa suka yi kuka ga Ubangiji saboda Midiyawa, 8 sai ya aika musu
da annabi, wanda ya ce, “Ga abin da Ubangiji, Allah na Isra’ila ya ce na fitar da ku
daga Masar, daga ƙasar bauta. 9 Na ƙwace ku daga ikon Masarawa da kuma daga
dukan hannuwan masu danniya. Na kore su a gabanku na kuma ba ku ƙasarsu.
10 Na ce muku, ‘Ni ne Ubangiji Allahnku; kada ku bauta allolin Amoriyawa, waɗanda
kuke zama a ƙasarsu.’ Amma ba ku saurare ni ba.”
11 Sai mala’ikan Ubangiji ya zo ya zauna a ƙarƙashin itacen oak a Ofra na Yowash
mutumin Abiyezer, inda ɗansa Gideyon yake sussukar alkama a wurin matsin inabi
don yă ɓoye daga Midiyawa. 12 Sa’ad da mala’ikan Ubangiji ya bayyana wa Gideyon,
sai ya ce masa, “Ubangiji yana tare da kai, jarumi.”
13 Gideyon ya ce, “Ranka yă daɗe, in Ubangiji yana tare da mu, me ya sa waɗannan
abubuwa suka faru da mu? Ina dukan abubuwan al’ajabinsa waɗanda kakanninmu
suka gaya mana game su sa’ad da suka ce, ‘Ashe, ba Ubangiji ne ya fitar da mu daga
Masar ba?’ Amma yanzu Ubangiji ya rabu da mu ya kuma sa mu hannun Midiyawa.”
14 Sai Ubangiji ya juya wajensa ya ce, “Ka je da ƙarfin da kake da shi ka ceci Isra’ila
daga hannun Midiyawa. Ba Ni ne nake aikan ka ba?”
15 Gideyon ya ce, “Amma Ubangiji,* yaya zan iya ceci Isra’ila? Kabilata ce marar
ƙarfi duka a Manasse, kuma ni ne ƙarami a iyalina.”
16 Ubangiji ya ce, “Zan kasance tare da kai, za ka kuwa fatattake dukan Midiyawa
gaba ɗaya.”
17 Gideyon ya ce, “In lalle na sami tagomashi a gabanka, to, ka ba ni wata alamar
da ta nuna lalle kai kake magana da ni. 18 Ina roƙonka ka dakata har in komo in
kawo maka hadayata in ajiye a gabanka.”
Sai Ubangiji ya ce, “Zan jira har ka dawo.”

* **6:15** Ko kuwa Ranka yă daɗe

19 Sai Gideyon ya shiga ciki, ya gyara ʼyar akuya ya dafa, da garin efa ya yi burodi
marar yisti. Da ya sa naman a kwando, romon kuma a tukunya, sai ya fito da su waje
ya miƙa masa su a ƙarƙashin itacen oak.
20 Malaʼikan Allah ya ce masa, "Ka ɗauko naman da burodi marar yisti ka sa su
a kan wannan dutse, ka zuba romon a kai." Gideyon kuwa ya yi haka. 21 Da kan
sandan da yake a hannunsa, malaʼikan Ubangiji ya taɓa naman da burodi marar
yistin. Sai wuta ta fito daga dutsen ta cinye naman da burodin. Malaʼikan kuwa ya
ɓace. 22 Saʼad da Gideyon ya gane malaʼikan Ubangiji ne, sai ya ce, "Ya Ubangiji Mai
Iko Duka! Na ga malaʼikan Ubangiji ido da ido."
23 Amma Ubangiji ya ce masa, "Salama! Kada ka ji tsoro, ba za ka mutu ba."
24 Saboda haka Gideyon ya gina wa Ubangiji bagade a can, ya kuma kira shi,
Ubangiji Salama ne. Har wa yau bagaden yana a Ofra ta mutanen Abiyezer.
25 A wannan dare Ubangiji ya ce masa, "Ka ɗauki bijimi na biyu daga garken
mahaifinka, wannan mai shekara bakwai.† Ka rushe bagaden mahaifinka na Baʼal
ka sare ginshiƙin Ashera‡ kusa da ita. 26 Saʼan nan ka gina bagade irin§ da ya dace
wa Ubangiji Allahnka a kan wannan tudu. Ka yi amfani da itacen katakon ginshiƙin
Ashera da ka sare, ka miƙa bijiman nan biyu hadaya ta ƙonawa."
27 Saboda haka Gideyon ya ɗebi bayinsa bakwai ya yi yadda Ubangiji ya ce masa.
Amma saboda yana tsoron iyalinsa da mutanen gari, ya yi haka da dare a maimako
da rana.
28 Da safe saʼad da mutanen garin suka tashi, sai suka tarar an rushe bagaden Baʼal,
tare da ginshiƙin Ashera da yake kusa da shi, duk an sare, bijimi na biyu kuma aka
miƙa hadaya a kan sabon bagaden!
29 Sai suka tambayi junansu, "Wa ya yi wannan?"
Saʼad da suka bincika a hankali, sai aka faɗa musu, "Gideyon ɗan Yowash ne ya yi
haka."
30 Mutanen garin suka ce wa Yowash, "Ka kawo mana ɗanka. Dole yǎ mutu, domin
ya rushe bagaden Baʼal, ya sare ginshiƙin Asheran da yake tsaye kusa da shi."
31 Amma Yowash ya ce wa taron da suka tayar masa, "Za ku yi hamayya domin Baʼal
ne? Kuna ƙoƙari ku cece shi ne? Duk wanda ya yi faɗa saboda shi za a kashe shi
kafin safe. In lalle Baʼal allah ne, zai kāre kansa saʼad da wani ya rushe bagadensa."
32 Saboda haka a ranar suka kira Gideyon, "Yerub-Baʼal,"* suna cewa, "Bari Baʼal ya
yi hamayya da shi," domin ya rushe bagaden Baʼal.
33 To, dukan Midiyawa, Amalekawa da sauran mutanen gabashi suka haɗa ƙarfi
suka ƙetare Urdun suka kafa sansani a Kwarin Yezireyel. 34 Saʼan nan Ruhun
Ubangiji ya sauko wa Gideyon, ya kuma busa ƙaho, ya kira mutanen Abiyezer su
bi shi. 35 Ya aika manzanni koʼina a Manasse, yana kiransu su kintsa, haka ma Asher,
Zebulun da Naftali, ta haka su ma suka haura su sadu da su.
36 Gideyon ya cewa Allah, "In za ka ceci Israʼila ta hannuna yadda ka yi alkawari,
37 to, zan shimfiɗa ulu a masussuka, inda safe akwai raɓa a kan ulun kaɗai, ƙasa
kuwa a bushe, to, zan san cewa za ka ceci Israʼila ta hannuna, yadda ka ce." 38 Abin
da faru ke nan. Gideyon ya tashi da sassafe kashegari, ya matse ulun ya kakkaɓe
raɓar, ruwan ya cika ƙwarya.
39 Saʼan nan Gideyon ya ce wa Allah, "Kada ka yi fushi da ni. Bari in ƙara yin wani
gwaji kuma da ulun. A wannan lokaci ka sa ulun yǎ bushe, ƙasar kuma ta rufu da
raɓa." 40 A wannan dare Allah ya yi haka. Ulun ne kaɗai yake a bushe, amma dukan
ƙasar ta jiƙe da raɓa.

---

† **6:25** Ko kuwa Ka ɗauki balagaggen bijimi wanda ya yi girma daga garken mahaifinka ‡ **6:25** Wato, alamar alliya Ashera; a nan da kuma koʼina a Mahukunta § **6:26** Ko kuwa ka gina da jerin duwatsu * **6:32** Yerub-Baal yana nufin bari Baʼal ya yi hamayya.

# 7

*Gideyon ya ci Midiyawa da yaƙi*

1 Kashegari da sassafe, Yerub-Ba'al (wato, Gideyon) da dukan mutanensa suka kafa
sansani a maɓulɓulan Harod. Sansanin Midiyawa kuma yana arewa da su a kwari
kusa da tudu na More. 2 Sai UBANGIJI ya ce wa Gideyon, “Mutanen da kake da su
sun yi mini yawa da zan ba da Midiyawa a hannunsu. Don kada Isra'ila tă yi mini
fahariya cewa ƙarfinta ne ya cece su, 3 ka yi shela ga mutane yanzu cewa, ‘Duk wanda
ya yi rawan jiki don tsoro, sai yă juya yă bar Dutsen Gileyad.’ ” Saboda haka mutum
dubu ashirin da biyu suka koma, sai mutum dubu goma suka rage.
4 Amma UBANGIJI ya ce wa Gideyon, “Har yanzu mutanen sun yi yawa. Ka kai cikin
ruwa, in kuma tankaɗe maka su a can. In na ce, ‘Wannan zai tafi da kai,’ to, zai tafi;
amma in na ce, ‘Wannan ba zai tafi da kai ba,’ to, ba zai tafi ba.”
5 Saboda haka Gideyon ya kai mutanen cikin ruwa. A can UBANGIJI ya ce masa, “Ka
ware waɗanda suka tanɗi ruwa kamar kare daga waɗanda suka durƙusa suka sha
ruwan.” 6 Mutum ɗari uku sun tanɗi ruwa, dukan sauran kuwa suka durƙusa suka
sha ruwan.
7 Sai UBANGIJI ya ce wa Gideyon, “Da mutum ɗari uku ɗin nan da suka tanɗi ruwa,
zan cece ka in kuma ba da Midiyawa a hannuwanku. Ka bar sauran mutane su
tafi kowa zuwa wurinsa.” 8 Saboda haka Gideyon ya mai da sauran Isra'ilawa zuwa
tentinsu amma ya riƙe mutum ɗari uku waɗanda suka karɓi guzuri da ƙahonin
sauran.
To, sansanin Midiyawa yana ƙasa da su a kwarin. 9 A daren nan UBANGIJI ya ce wa
Gideyon, “Tashi ka tafi sansaninsu domin zan ba da su a hannuwanka. 10 In kana
tsoron fāɗa musu, sai ka tafi da bawanka Fura 11 ka kuma saurari abin da suke faɗi.
Bayan haka za ka sami ƙarfin hali ka auka musu.” Saboda haka sai ya tafi tare da
Fura bawansa zuwa sansanin. 12 Midiyawa, Amalekawa da dukan sauran mutane
gabashi suka yi sansani a kwari, kamar fāra. Raƙumansu kuma kamar yashi a bakin
teku don sun wuce ƙirge.
13 Gideyon ya iso daidai wani yana faɗa wa wani aboki mafarkinsa, yana cewa,
“Na yi mafarki, na ga dunƙule burodin sha'ir ya fāɗo a tsakiyar sansanin Midiyawa.
Ya bugi tentin da ƙarfin da ya sa tenti ta kife a ƙasa.”
14 Abokinsa ya ce, “Ai wannan ba wani abu ba ne fiye da takobin Gideyon
ɗan Yowash, mutumin Isra'ila. Allah ya ba da Midiyawa da dukan sansani a
hannuwansa.”
15 Da Gideyon ya ji mafarkin da fassararsa, sai ya yi wa Allah sujada. Ya koma
sansanin Isra'ila ya yi kira da ƙarfi ya ce, “Ku tashi! UBANGIJI ya ba da sansanin
Midiyawa a hannuwanku.” 16 Ya raba mutum ɗari uku ɗin kashi uku, ya ba
kowannensu ƙaho da tulu da acibalbal a ciki.
17 Ya ce musu, “Ku dube ni, ku bi abin da na yi. Sa'ad da na kai sansanin, ku yi
daidai abin da na yi. 18 Sa'ad da ni da dukan waɗanda suke tare da ni muka busa
ƙahoninmu, to, ko'ina a kewayen sansanin sai ku busa naku ku kuma yi ihu, ku ce,
‘Don UBANGIJI da kuma domin Gideyon.’ ”
19 Gideyon da mutum ɗari da suke tare da shi suka kai sansanin da tsakar dare
bayan an sauya matsara. Suka busa ƙahoninsu, suka farfashe tulunansu da suke
hannuwansu. 20 Kungiyoyi uku ɗin nan suka busa ƙahonin, suka fasa tuluna. Suka
ɗauki acibalbal a hannuwansu na hagu da ƙahonin busawa a hannuwansu na dama,
sai suka yi ihu, “Takobi don UBANGIJI da kuma don Gideyon!” 21 Yayinda kowannensu
ya tsaya a inda yake kewaye da sansanin, dukan Midiyawa suka fito da gudu, suna
kuka yayinda suke gudu.
22 Sa'ad da aka busa ƙahonin nan ɗari uku sai UBANGIJI ya sa Midiyawa suka yi
ta saran juna. Mayaƙan suka gudu zuwa Bet-Shitta wajen Zerera har zuwa yankin

Abel-Mehola kusa da Tabbat. 23 Aka kira dukan Isra'ilawa daga Naftali, Asher da
dukan Manasse, suka kuwa fatattaki Midiyawa. 24 Gideyon ya aiki manzanni zuwa
dukan ƙasar tudu ta Efraim cewa, “Ku gangaro ku yaƙi Midiyawa ku ƙwace ruwan
Urdun gaba da su har zuwa Bet-Bara.”

Saboda haka aka kira dukan mutanen Efraim suka ƙwace ruwan Urdun har zuwa
Bet-Bara. 25 Suka kuma kama shugabannin biyu na Midiyawa, Oreb da Zeyib suka
kashe Oreb a dutsen Oreb, Zeyib kuma a wurin matsin ruwa inabin Zeyib. Suka
fatattaki Midiyawa suka kawo kawunan Oreb da Zeba wurin Gideyon, wanda yake
kusa da Urdun.

# 8

*Zeba da Zalmunna*

1 To, mutanen Efraim suka ce wa Gideyon, “Me ya sa ka yi mana haka? Me ya sa
ba ka kira mu lokacin da ka tafi yaƙi da Midiyawa ba?” Suka zarge shi sosai.

2 Amma ya ce musu, “Me na yi da za a iya kwatanta da abin da kuka yi? Ashe, kalar
inabin da Efraim ta yi bai fi dukan girbin inabin da Abiyezer suka yi ba? 3 Allah ya
ba da Oreb da Zeyib, shugabannin Midiyawa a hannuwanku. Me na yi da ya fi naku?
Da ya faɗi haka sai hankalinsu ya kwanta.”

4 Gideyon da mutanensa ɗari uku, sun gaji, duk da haka suka yi ta fafarar, suka zo
Urdun suka haye shi. 5 Ya ce wa mutanen Sukkot, “Ku ba wa mutanena burodi; sun
gaji, har yanzu ina fafarar Zeba da Zalmunna, sarakunan Midiyawa.”

6 Amma shugabannin Sukkot suka ce, “Ka kama Zeba da Zalmunna ko ne? Don me
za mu ba wa mayaƙanka burodi?”

7 Sai Gideyon ya ce, “Haka ko? To, sa'ad da Ubangiji ya ba da Zeba da Zalmunna a
hannuna, zan tsattsaga jikinku da ƙayayyuwan jeji.”

8 Daga nan ya wuce zuwa Fenuwel ya yi irin roƙon nan, amma suka amsa yadda
mutanen Sukkot suka yi. 9 Saboda haka sai ya ce wa mutanen Fenuwel, “Sa'ad da na
dawo da nasara zan rushe wannan hasumiya.”

10 To, Zeba da Zalmunna suna a Karkor da mayaƙa wajen dubu goma sha biyar,
abin da ya rage ke nan na mayaƙan gabashi; mayaƙa masu takobi dubu ɗari da
ashirin ne suka mutu. 11 Gideyon ya haura ta hanyar makiyaya, gabas da Noba, da
kuma Yogbeha, ya fāɗa wa mayaƙan ta yadda ba su zata ba. 12 Zeba da Zalmunna,
sarakunan biyu na Midiyawa suka tsere, amma ya bi su ya kama, ya fatattaki dukan
mayaƙansu.

13 Sa'an nan Gideyon ɗan Yowash ya komo daga yaƙi ta Hanyar Heres. 14 Ya kama
wani saurayin Sukkot ya tambaye shi, saurayin kuwa ya rubuta masa dukan sunayen
shugabanni saba'in da bakwai na Sukkot, da dattawan garin. 15 Sa'an nan Gideyon ya
zo ya ce wa mutanen Sukkot, “To, ga Zeba da Zalmunna, waɗanda kuka yi mini ba'a
kuna cewa, ‘Ka kama Zeba da Zalmunna ko ne? Me zai sa mu ba mutanenka da suka
gaji burodi?’ ” 16 Ya kwashe dattawan garin ya koya wa mutanen Sukkot hankali ta
wurin hukunta su da ƙayayyuwan hamada. 17 Ya rushe hasumiyar Fenuwel ya kuma
karkashe mutanen garin.

18 Sa'an nan ya ce wa Zeba da Zalmunna, “Waɗanne irin mutane ne kuka karkashe
a Tabor.”

Suka ce, “Mutane kamar ka ne kowane kamar ɗan sarki.”

19 Gideyon ya ce, “Waɗannan 'yan'uwana ne, 'ya'yan mahaifiyata. Muddin
Ubangiji yana a raye, da a ce kun bar su da rai, da ba zan kashe ku ba.” 20 Da
ya juya wajen Yeter, ɗan farinsa, sai ya ce, “Ka kashe su!” Amma Yeter bai zāre
takobinsa ba, domin shi yaro ne kawai kuma yana tsoro.

21 Zeba da Zalmunna suka ce masa, “Zo, ka yi da kanka. ‘Yadda mutum yake haka
ƙarfinsa.’ ” Ta haka Gideyon ya matso gaba ya kashe su, ya ɗauki kayan ado daga
wuyar raƙumansu.

*Efod na Gideyon*

22 Isra’ilawa suka ce wa Gideyon, “Ka yi mulkinmu, kai, ɗanka da jikanka, domin
ka cece mu daga hannun Midiyawa.”
23 Amma Gideyon ya ce musu, “Ni, ko ɗana, ba za mu yi mulkinku ba. UBANGIJI ne
zai yi mulkinku.” 24 Kuma ya ce, “Ina da roƙo guda ɗaya, cewa kowannenku ya ba ni
’yan kunne daga rabon ganima.” (Al’adar mutanen Ishmayel ce su sa ’yan kunnen
zinariya.)
25 Suka ce, “Za mu yi farin cikin ba ka su.” Saboda haka suka shimfiɗa mayafi,
kowanne ya sa ɗan kunne ɗaya daga ganimar. 26 Nauyin ’yan kunnen zinariyar ya
kai shekel ɗari goma sha bakwai, ban da kayan ado, abin wuya da tufafin shunayya
waɗanda sarakuna Midiyawa suke sawa ko sarƙoƙin da suke wuyar raƙumansu.
27 Gideyon ya efod da zinariyar, wanda ya ajiye a Ofra, garinsa. Dukan Isra’ila suka
shiga yin karuwanci ta wurin yin sujada a can, ya kuwa zama wa Gideyon da dukan
iyalinsa tarko.

*Rasuwar Gideyon*

28 Da haka Isra’ilawa suka mallaki Midiyawa ba su kuma sāke tā da kai ba. A
zamanin Gideyon ƙasar ta sami zaman lafiya har shekara arba’in.
29 Yerub-Ba’al ɗan Yowash ya koma gida don yǎ zauna. 30 Yana da ’ya’ya saba’in
maza da ya haifa, gama yana da mata da yawa. 31 Yana kuma da ƙwarƙwara wadda
take Shekem, ita ma ta haifa masa ɗa wanda ya ba shi suna Abimelek. 32 Gideyon
ɗan Yowash ya rasu da kyakkyawan tsufa aka kuma binne shi a kabarin Yowash
mahaifinsa a Ofra na mutanen Abiyezer.
33 Ba a daɗe da rasuwar Gideyon ba, sai Isra’ila ta sāke shiga karuwanci suna
bauta wa Ba’al. Suka kafa Ba’al-Berit yǎ zama musu allahnsu ba kuma 34 tuna da
UBANGIJI Allahnsu, wanda ya cece su daga hannuwan abokan gābansu a kowane gefe
ba. 35 Suka kāsa nuna alheri ga gidan Yerub-Ba’al (wato, Gideyon) saboda abubuwa
masu alherin da ya yi musu.

# 9

*Abimelek*

1 Abimelek ɗan Yerub-Ba’al ya tafi Shekem wurin ’yan’uwan mahaifiyarsa, ya
ce musu da kuma dukan dangin mahaifiyarsa, 2 “Ku tambayi ’yan ƙasar Shekem,
‘Wanne ya fi muku, a sa dukan ’ya’yan Yerub-Ba’al saba’in maza su yi mulkinku, ko
dai mutum guda kawai yǎ yi mulkinku?’ Ku tuna, ni jininku ne.”
3 Sa’ad da ’yan’uwan suka mayar wa ’yan ƙasar Shekem wannan, sai suka goyi
bayan Abimelek, gama sun ce, “Shi ɗan’uwanmu ne.” 4 Suka ba shi shekel saba’in
na azurfa daga haikalin Ba’al-Berit, Abimelek kuwa ya yi amfani da shi ya yi hayar
’yan tauri waɗanda suka zama masu binsa. 5 Sai ya tafi gidan mahaifinsa a Ofra
kuma a dutse guda ya kashe ’yan’uwansa, ’ya’yan Yerub-Ba’al. Amma Yotam, autan
ɗan Yerub-Ba’al ya tsira ta wurin ɓuya. 6 Sa’an nan duka ’yan ƙasar Shekem da Bet
Millo suka taru kusa da babban itacen wajen ginshiƙi a Shekem don a naɗa Abimelek
sarki.
7 Sa’ad da aka gaya wa Yotam wannan, sai ya hau Dutsen Gerizim ya yi kira da
ƙarfi ya ce, “Ku saurare ni, ’yan ƙasar Shekem, don Allah yǎ saurare ku. 8 Wata rana
itatuwa suka fita don su naɗa wa kansu sarki. Suka ce wa itacen zaitun, ‘Ka zama
sarkinmu.’

9 “Amma itacen zaitun ya ce, ‘In bar mai nawa, wanda da shi ake girmama alloli
da mutane, don in zo in yi ta fama da itatuwa?’
10 “Biye da wannan, sai itatuwan suka ce wa itacen ɓaure, ‘Zo ka zama sarkinmu.’
11 “Amma itacen ɓauren ya ce, ‘In bar kyawawan ’ya’yana da zaƙinsu, in zo in yi
ta fama da itatuwa?’
12 “Sa’an nan itatuwan suka ce wa kuringar inabi, ‘Ki zo ki zama sarkinmu.’
13 “Amma kuringar ta ce, ‘In bar ruwan inabina, wanda yake faranta zuciyar alloli
da mutane, in zo in yi fama da itatuwa?’
14 “A ƙarshe sai dukan itatuwa suka ce wa itacen ƙaya, ‘Ka zo ka zama sarkinmu.’
15 “Itacen ƙaya ya ce wa itatuwan, ‘In da gaske ne kuke so ku naɗa ni sarkinku, ku
zo ku sha inuwana; in ba haka ba, bari wuta ta fito daga itacen ƙaya ta cinye itacen
al’ul na Lebanon!’
16 “To, da a ce kun yi abin bangirma da aniya mai kyau sa’ad da kuka naɗa
Abimelek sarki, da kun nuna wa Yerub-Ba’al da iyalinsa ladabi, da kuma kun yi
masa abin da ya cancanci shi, 17 a yi tunani cewa mahaifina ya yi yaƙi saboda ku, ya
yi kasai da ransa don yǎ cece ku daga hannun Midiyawa 18 (amma ga shi yau kun
tayar wa iyalin mahaifina, kuka kashe ’ya’yansa saba’in a dutse guda, kuka kuma
naɗa Abimelek, ɗan baiwa, sarki a kan ’yan ƙasar Shekem domin shi ɗan’uwanku
ne) 19 in har kun aikata wannan cikin bangirma da kuma aminci wajen Yerub-Ba’al
da iyalinsa a yau, bari Abimelek yǎ zama farin cikinku, ku kuma nasa! 20 Amma
in ba haka ba, bari wuta ta fito daga Abimelek ya cinye ku, ’yan ƙasar Shekem da
Bet Millo, bari wuta kuma daga wurinku ’yan ƙasar Shekem da Bet Millo ta cinye
Abimelek!”
21 Sa’an nan Yotam ya gudu, ya tsere zuwa Beyer ya zauna a can gama yana tsoron
ɗan’uwansa Abimelek.
22 Bayan Abimelek ya yi shekara uku yana mulki a Isra’ila, 23 sai Allah ya aiko
da mugun ruhu tsakanin Abimelek da ’yan ƙasar Shekem, waɗanda suka ci amanar
Abimelek. 24 Allah ya yi haka saboda kisan ’ya’ya saba’in na Yerub-Ba’al, don a ɗauki
fansar jininsu a kan Abimelek ɗan’uwansu da kuma ’yan ƙasar Shekem, waɗanda
suka taimake shi kisan ’yan’uwansa. 25 Cikin hamayya da shi waɗannan ’yan ƙasar
Shekem suka sa mutane a kan tuddai don su yi kwanton ɓauna a kan su yi fashi ga
duk wanda ya wuce a can, wannan fa ya kai kunnen Abimelek.
26 To, Ga’al ɗan Ebed ya tafi tare da ’yan’uwansa zuwa Shekem, ’yan ƙasarta kuwa
suka dogara da shi. 27 Bayan sun tafi gonaki suka tattara inabi suka matse su, sai
suka yi biki a haikalin allahnsu. Yayinda suke ci da sha, sai suka la’anci Abimelek.
28 Sa’an nan Ga’al ɗan Ebed ya ce, “Wane ne Abimelek, kuma wane ne Shekem, da za
mu bauta masa? Shi ba ɗan Yerub-Ba’al ba ne, kuma ba Zebul ne mataimakinsa ba?
Ku bauta wa mutanen Hamor, mahaifin Shekem! Me ya sa za mu bauta wa Abimelek?
29 Da a ce waɗannan mutane suna a ƙarƙashina mana! Da zan hamɓarar da shi. In
ce wa Abimelek, ‘Ka tara dukan mayaƙanka!’ ”
30 Sa’ad da Zebul gwamnar birnin ya ji abin da Ga’al ɗan Ebed ya ce, sai ya fusata.
31 Asirce sai ya aiki manzanni wajen Abimelek, yana cewa, “Ga’al ɗan Ebed da
’yan’uwansa sun zo Shekem suna kuma zuga birnin sun tayar maka. 32 To, in dare
ya yi, sai ka zo da mutanenka ku yi kwanto a filaye. 33 Kashegari da safe, sai ku tashi
ku fāɗa wa birnin. Sa’ad da Ga’al da mutanensa suka faɗa maka, sai ka yi abin da
ka iya yi da su.”
34 Saboda haka Abimelek da dukan mutanensa suka tashi da dare suka ɓuya kusa
da Shekem a ƙungiyoyi huɗu. 35 To, Ga’al ɗan Ebed ya riga ya fita waje yana tsaye a
ƙofar birni daidai Abimelek da mayaƙansa suka fito daga inda suka ɓuya.
36 Sa’ad da Ga’al ya gan su, sai ya ce wa Zebul, “Duba, ga mutane suna gangarowa
daga kan duwatsu!”

Zebul ya ce, “Kana ɗaukan inuwan duwatsu kana ce mutane.”
37 Amma Ga’al ya sāke magana ya ce, “Duba, mutane suna gangarowa daga tsakiyar
filaye, kuma wata ƙungiya tana zuwa daga wajen itacen masu duba.”
38 Sa’an nan Zebul ya ce masa, “Ina bakin da ka yi ɗin, kai da ka ce, ‘Wane ne
Abimelek da za mu bauta masa.’ Ba mutanen ne ka yi musu ba’a ba? Fita, ka yaƙe
su mana!”
39 Saboda haka Ga’al ya fito da ’yan ƙasar Shekem suka yaƙi Abimelek. 40 Abimelek
ya kore shi, mutane da yawa suka ji ciwo a yaƙin, har zuwa ƙofar birnin. 41 Abimelek
ya zauna a Aruma, Zebul kuwa ya kori Ga’al da ’yan’uwansa daga Shekem.
42 Kashegari mutanen Shekem suka tafi gonaki, aka kuwa gaya wa Abimelek.
43 Saboda haka ya ɗauki mutanensa, ya raba su ƙungiya uku, sa’an nan ya yi kwanto
a gonakin. Sa’ad da ya ga mutanen suna fitowa daga birni, sai ya yi wuf ya fāɗa
musu. 44 Abimelek da ƙungiyoyin da suke tare da shi suka yi maza suka yi tsaya
a ƙofar birnin. Sa’an nan ƙungiyoyi biyu suka ruga suka fāɗa wa waɗanda suke a
gonaki suka karkashe su. 45 Dukan yinin, Abimelek ya matsa yaƙi da birnin sai da ya
cinye ta ya kuma kashe mutanenta. Sa’an nan ya hallaka birnin ya barbaza gishiri a
kanta.
46 Da jin haka, sai ’yan ƙasa a hasumiyar Shekem suka shiga wurin mafaka a
hankalin El-Berit. 47 Da Abimelek ya ji dukan mutanen hasumiyar Shekem sun taru
a can, 48 sai Abimelek da dukan mutanensa suka haura zuwa Dutsen Zalmon. Sai
ya ɗauki gatari ya sassare waɗansu rassa, waɗanda ya sa a kafaɗunsa. Ya umarci
mutanen da suke tare da shi ya ce, “Sauri, ku yi abin da kuka ga na yi!” 49 Saboda
haka mutanen suka sassare rassan itatuwa suka bi Abimelek. Suka tattara su a jikin
mafakar suka kuma cinna mata wuta a kan mutanen da suke a ciki. Ta haka dukan
mutanen da suke cikin hasumiyar Shekem, wajen maza da mata dubu ɗaya suka
mutu.
50 Biye da wannan Abimelek ya tafi Tebez, ya kewaye ta ya kuma cinye ta da yaƙi.
51 A cikin birnin, akwai wata hasumiya mai ƙarfi, inda dukan maza da mata, dukan
mutanen birnin, suka ɓuya. Suka kulle kansu, suka kuma hau rufin hasumiyar.
52 Abimelek ya je wajen hasumiya ya kuma auka mata. Amma da ya yi kusa da ƙofar
hasumiyar don yǎ cinna mata wuta, 53 sai wata mata ta saki ɗan dutsen niƙa a kan
Abimelek ta fasa ƙoƙon kansa.
54 Da sauri ya kira mai riƙon masa makami ya ce, “Zaro takobinka ka kashe ni,
don kada a ce ‘Mace ce ta kashe shi.’ ” Saboda haka bawansa ya soke shi, ya mutu.
55 Sa’ad da Isra’ilawa suka ga Abimelek ya mutu, sai suka tafi gida.
56 Ta haka Allah ya sāka muguntar da Abimelek da ya yi wa mahaifinsa ta wurin
kisan ’yan’uwansa saba’in. 57 Allah kuma ya sa muguntar mutanen Shekem suka
koma kansu. La’anar Yotam ɗan Yerub-Ba’al kuma ta kama su.

# 10

### *Tola*

1 Bayan zamanin Abimelek, sai Tola ɗan Fuwa ɗan Dodo daga Issakar ya tashi don
yǎ ceci Isra’ila. Yana zama a Shamir a ƙasar tudu ta Efraim. 2 Ya shugabanci Isra’ila
shekara ashirin da uku sa’an nan ya mutu, aka kuma binne shi a Shamir.

### *Yayir*

3 Bayansa kuma sai Yayir daga Gileyad, wanda ya shugabanci Isra’ila shekara
ashirin da biyu. 4 Yana ’ya’ya talatin, waɗanda suke hawan jakuna talatin. Sun
shugabanci birane talatin a Gileyad, har wa yau ana ce da biranen Hawwot Yayir.*
5 Sa’ad da Yayir ya mutu, sai aka binne shi a Kamon.

* **10:4** Ko kuwa ana ce da su mazaunan Yayir

*Yefta*

6 Isra'ilawa suka sāke yin mugayen ayyuka a gaban UBANGIJI. Suka shiga bautar
Ba'al da Ashtarot, da kuma allolin Aram, allolin Sidon, allolin Mowab, Ammonawa da
kuma allolin Filistiyawa. Kuma domin Isra'ilawa sun bar UBANGIJI ba su ƙara bauta
masa ba, 7 sai ya fusata da su. Ya sayar da su ga hannun Filistiyawa da Ammonawa,
8 waɗanda suka fatattake su a shekarar suka kuma ragargaza su. Shekara goma sha
takwas suka yi ta danne dukan Isra'ilawan da suke gabashin Urdun a Gileyad, ƙasar
Amoriyawa. 9 Ammonawa su ma suka haye Urdun domin su yi yaƙi da Yahuda,
Benyamin da kuma gidan Efraim; Isra'ila kuwa suka kasance cikin wahala ƙwarai
da gaske. 10 Sa'an nan Isra'ilawa suka yi kuka ga UBANGIJI, suka ce, "Mun yi maka
zunubi, mun bar Allahnmu muka shiga bautar Ba'al."

11 UBANGIJI ya ce, "Sa'ad da Masarawa, Amoriyawa, Ammonawa, Filistiyawa,
12 Sidoniyawa, Amalekawa da kuma mutanen Mawon suka wulaƙanta ku kuka kuwa
yi mini kuka, ban cece ku daga hannunsu ba? 13 Amma kuka bar ni kuka bauta wa
waɗansu alloli, saboda haka ni ma ba zan ƙara cece ku ba. 14 Ku tafi ku yi wa allolin
da kuka zaɓa. Bari su cece ku sa'ad da kuke cikin wahala!"

15 Amma Isra'ilawa suka ce wa UBANGIJI, "Mu dai mun yi zunubi. Ka yi da mu abin
da ka ga dama, amma muna roƙonka ka cece mu a yanzu." 16 Sa'an nan suka zubar
da allolin nan daga cikinsu suka bauta wa UBANGIJI. UBANGIJI kuwa bai ƙara daure
da azabar da Isra'ila suke sha ba.

17 Sa'ad da aka kira Ammonawa su yi ɗamarar yaƙi, sai su kuma kafa sansani
a Gileyad, Isra'ilawa kuwa suka tattaru suka kafa sansani Mizfa. 18 Shugabannin
mutanen Gileyad suka cewa juna, "Duk wanda zai fara fāɗa wa Ammonawa shi zai
zama shugaban duk waɗanda suke zama a Gileyad."

# 11

1 Yefta mutumin Gileyad, jarumi ne ƙwarai. Mahaifinsa ne Gileyad; mahaifiyar
kuwa karuwa ce. 2 Matar Gileyad ta haifa masa 'ya'ya maza, kuma sa'ad da suka yi
girma, sai suka kore Yefta, suka ce "Ba ka da gādo a cikin iyalinmu, domin kai ɗan
wata mace ce." 3 Saboda haka Yefta ya tsere daga 'yan'uwansa ya zauna a ƙasar Tob,
inda waɗansu 'yan iska suka kewaye shi suka bi shi.

4 Ana nan, sa'ad da Ammonawa suka kai wa Isra'ilawa hari, 5 dattawan Gileyad
suka je suka nemo Yefta daga ƙasar Tob. 6 Suka ce masa, "Ka zo ka zama mana
shugaba, don mu yaƙi Ammonawa."

7 Yefta ya ce musu, "Ba kun ƙi ni kuka kuma kore ni daga gidan mahaifina ba? Me
ya sa kuke zuwa wurina yanzu sa'ad da kuke cikin wahala?"

8 Mutanen Gileyad suka ce masa, "Duk da haka, muna juyo wajenka yanzu, ka zo
tare da mu mu yaƙi Ammonawa, za ka kuma zama shugaban duk wanda yake zama
a Gileyad."

9 Yefta ya ce, "A ce kun dawo da ni in yaƙi Ammonawa, UBANGIJI kuwa ya ba da su
a hannuna, zan zama shugabanku?"

10 Dattawan Gileyad suka ce, "UBANGIJI ne shaidanmu; za mu yi duk abin da ka
ce." 11 Saboda haka Yefta ya tafi tare da dattawan Gileyad, mutanen kuwa suka naɗa
shi shugabansu da kuma sarkinsu. Ya kuwa maimaita dukan maganarsa a gaban
UBANGIJI a Mizfa.

12 Sa'an nan Yefta ya aiki jakadu zuwa wurin sarkin Ammonawa su tambaya, "Me
ya haɗa ka da ni, da ka kawo wa ƙasata yaƙi?"

13 Sarkin Ammonawa ya ce wa jakadu, "Sa'ad da Isra'ilawa suka fito daga Masar,
sun ƙwace mini ƙasa tun daga Arnon zuwa Yabbok, har zuwa Urdun. Yanzu ka
mayar mini ita cikin salama."

14 Yefta ya sāke aikan jakadu wurin sarki, 15 yana cewa,
“Ga abin da Yefta yake faɗi, Isra’ila ba tă ƙwace ƙasar Mowab ko ta Ammonawa
ba. 16 Amma sa’ad da suka bar Masar, Isra’ila ta bi ta hamada zuwa Jan Teku* har
suka zo Kadesh. 17 Sa’an nan Isra’ila ta aiki jakadu zuwa ga sarkin Edom cewa,
‘Ka ba mu izini mu ratsa ƙasarka,’ amma sarkin Edom bai saurara ba. Suka kuma
aika wa sarkin Mowab, shi ma ya ƙi. Saboda haka Isra’ila ta zauna a Kadesh.
18 “Daga can suka ci gaba ta hamada, suka zaga ƙasashen Edom da Mowab, suka
wuce ta gabashin ƙasar Mowab, sa’an nan suka yi sansani a ɗaya gefen Arnon. Ba
su shiga yankin Mowab ba, gama Arnon ce iyakarta.
19 “Sa’an nan Isra’ila ta aiki jakadu zuwa ga Sihon sarkin Amoriyawa, wanda
yake mulki a Heshbon, ta ce masa, ‘Ka bar mu mu ratsa ƙasarka mu wuce zuwa
wurinmu.’ 20 Sihon dai, bai amince da Isra’ila su ratsa ƙasarsa ba. Ya tattara dukan
mutanensa suka yi sansani a Yahza suka kuwa yaƙi Isra’ila.
21 “Sa’an nan Ubangiji, Allah na Isra’ila, ya ba da Sihon da dukan mutanensa
a hannun Isra’ila, suka kuwa ci nasara a kansu. Isra’ila ta ƙwace dukan ƙasar
Amoriyawa da suke zaune a ƙasar, 22 suka ƙwace dukan yankin Amoriyawa tun
daga ƙasar Arnon zuwa Yabbok, daga hamada har zuwa Urdun.
23 “To, da yake Ubangiji, Allah na Isra’ila, ya kori Amoriyawa a gaban mutanensa
Isra’ila, wane ’yanci kake da shi da za ka karɓe ta? 24 Ba za ka karɓi abin da
allahnka Kemosh ya ba ka ba? Haka mu ma, duk abin da Ubangiji Allahnmu ya
riga ya ba mu, za mu mallake shi. 25 Ka fi Balak ɗan Ziffor, sarkin Mowab ne? Ka
taɓa ji ya yi hamayya da Isra’ila ko yă yi yaƙi da su? 26 Shekara ɗari uku Isra’ilawa
suka yi zamansu a Heshbon, Arower da ƙauyukan kewayenta da dukan biranen da
suke gefen Arnon. Me ya sa ba ka karɓe su a lokacin ba? 27 Ban yi maka laifi ba,
amma kana musguna mini ta wurin kawo mini hari. Bari Ubangiji yă zama Alƙali,
yă yanke hukunci tsakani Isra’ilawa da Ammonawa.”
28 Duk da haka sarkin Ammonawa bai kula da saƙon da Yefta ya aika ba.
29 Sa’an nan Ruhun Ubangiji ya sauko wa Yefta. Sai ya haye Gileyad da Manasse,
ya ratsa ta Mizfa zuwa Gileyad, daga can kuma ya kai wa Ammonawa hari. 30 Yefta
kuwa ya yi wa’adi da Ubangiji ya ce, “In ka ba da Ammonawa a hannuwana, 31 duk
abin da ya fara fitowa daga ƙofar gidana don yă tarye ni, sa’ad da na komo daga yaƙi
da Ammonawa, zai zama na Ubangiji, zan miƙa shi hadaya ta ƙonawa.”
32 Sa’an nan Yefta ya haye zuwa wajen Ammonawa don yaƙi da su. Ubangiji kuwa
ya ba da su a hannuwansa. 33 Ya hallaka birane ashirin tun daga Arower zuwa yankin
Minnit, har zuwa Abel-Keramim. Haka Isra’ila ta cinye Ammonawa ƙaf.
34 Sa’ad da Yefta ya komo gida a Mizfa, wa ya fito yă tarye shi, ’yarsa tilo, tana rawa
kiɗin ganguna! Ita ce kaɗai ’yarsa. Ban da ita ba shi da ɗa ko ’ya. 35 Da ya gan ta,
sai ya yayyage tufafinsa ya yi kuka ya ce, “Kaito! ’Yata! Kin karya mini gwiwa, kuma
na lalace, domin na yi wa’adi ga Ubangiji da ba zan iya in karya ba.”
36 Ta ce, “Mahaifina, idan ka riga ka yi wa Ubangiji magana, sai ka yi da ni yadda
ka yi alkawari, da yake Ubangiji ya ɗau maka fansa a kan Ammonawa.” 37 Sai ta
kuma ce, “Sai dai, ka biya mini wannan bukata guda. Ka ba ni wata biyu in yi ta
yawo da ni da ƙawayena a kan duwatsu mu yi makoki, domin ba zan yi aure ba.”
38 Ya ce mata, “Ki tafi,” Ya bar ta tă tafi har wata biyu. Ita da ’yan matan suka tafi a
kan duwatsu suka yi ta makoki domin ba za tă taɓa aure ba. 39 Bayan watanni biyu
ɗin sai ta komo wurin mahaifinta ya kuwa yi da ita yadda ya yi wa’adi. Ita kuwa ba
tă taɓa san namiji ba.
Wannan ya zama al’ada a Isra’ila, 40 cewa kowace shekara ’yan mata sukan fita
kwana huɗu don yin bikin tunawa da ’yar Yefta mutumin Gileyad.

* **11:16** Da Ibraniyanci Yam Suf; wato, Tekun Iwa.

# 12

*Yefta da Efraim*

1 Mutanen Efraim suka tattaro mayaƙansu, suka haye zuwa Zafon suka cewa Yefta, "Don me ka tafi ka yaƙi Ammonawa ba ka gayyace mu ba? Za mu ƙone gidanka a kanka."
2 Yefta ya ce, "Ni da mutanena mun yi ta jayayya sosai da Ammonawa, ko da yake
na kira ku, amma ba ku cece ni daga hannuwansu ba. 3 Da na ga ba za ku taimake
ni ba, sai na yi kasai da raina na kuwa haye don in yaƙi Ammonawa, UBANGIJI kuwa ya ba ni nasara a kansu. To, don me kuka zo yau don ku yaƙe ni?"
4 Sa'an nan Yefta ya tara mutanen Gileyad wuri guda ya kuma yaƙi Efraim. Mutanen Gileyad suka fatattake su domin mutanen Efraim sun ce, "Ku Mutanen
Gileyad masu neman mafaka ne cikin Efraim da Manasse." 5 Mutanen Gileyad suka
ƙwace mashigan Urdun masu zuwa Efraim, duk sa'ad da wani daga Efraim da ya tsira ya ce, "Bari in haye," sai mutane Gileyad su ce "Kai mutumin Efraim ne?" In
ya ce, "A'a," 6 sai su ce, "To, ka ce, 'Shibbolet.' " In ya ce, "Sibbolet," saboda ba sa iya faɗin kalmar daidai, sai su kama shi su kashe a mashigan Urdun. Aka kashe mutanen Efraim dubu arba'in da biyu a ta haka.
7 Yefta ya shugabanci Isra'ila shekara shida. Sa'an nan Yefta mutumin Gileyad ya mutu, aka kuwa binne shi wani gari a Gileyad.

*Ibzan, Elon da Abdon*

8 Bayansa, Ibzan mutumin Betlehem, ya shugabanci Isra'ila. 9 Yana 'ya'ya maza
talatin da 'ya'ya mata talatin. Ya ba da auren 'ya'yansa mata ga waɗanda ba daga dangi ba, ga 'ya'yansa maza kuwa ya kawo 'yan mata talatin su zama matansu waje
da danginsa. Ibzan ya shugabanci Isra'ila shekara bakwai. 10 Sa'an nan Ibzan ya
mutu, aka kuwa binne shi Betlehem.
11 Bayansa, Elon mutumin Zebulun, ya shugabanci Isra'ila shekara goma. 12 Sa'an
nan Elon ya mutu, aka kuwa binne shi a Aiyalon a ƙasar Zebulun.
13 Bayansa, Abdon ɗan Hillel, daga Firaton, ya shugabanci Isra'ila. 14 Yana da 'ya'ya
maza arba'in da 'yan taɓa kunne talatin, waɗanda suka hau jakuna saba'in. Ya
shugabanci Isra'ila shekara takwas. 15 Sa'an nan Abdon ɗan Hillel ya mutu, aka
kuwa binne shi a Firaton a Efraim, a ƙasar tudu ta Amalekawa.

# 13

*Haihuwar Samson*

1 Isra'ilawa suka sāke yin mugayen ayyuka a gaban UBANGIJI, saboda haka ya ba
da su a hannun Filistiyawa shekara arba'in.
2 Akwai wani mutumin Zora, mai suna Manowa, daga kabilar Dan, matarsa kuwa
bakararriya ce, ba ta haihuwa. 3 Mala'ikan UBANGIJI ya bayyana gare ta ya ce, "Ga
shi ke bakararriya ce ba kya haihuwa, amma za ki yi ciki ki kuma haifi ɗa. 4 To, sai
ki lura kada ki sha ruwan inabi ko wani abu mai sa maye, kada kuma ki ci wani abu
marar tsarki, 5 gama za ki yi ciki, ki haifi ɗa. Aska ba za tă taɓa kansa ba, domin
yaron zai zama Banazare, keɓaɓɓe ga Allah tun daga haihuwa, shi ne kuwa zai soma
ceton Isra'ilawa daga hannuwan Filistiyawa."
6 Sa'an nan matar ta tafi wajen mijinta ta faɗa masa cewa, "Wani mutumin Allah
ya zo wurina. Ya yi kama da mala'ikan Allah, yana da bantsoro ƙwarai. Ban tambaye
shi inda ya fito ba, kuma bai gaya mini sunansa ba. 7 Sai dai ya ce mini, 'Za ki yi ciki,
ki kuma haifi ɗa. To, fa, kada ki sha ruwan inabi ko abu mai sa maye kada kuma ki ci abin da yake marar tsarki, gama ɗan zai zama Banazare na Allah tun daga haihuwa har ranar mutuwarsa.' "

8 Sai Manowa ya yi addu'a ga Ubangiji ya ce, "Ya Ubangiji, ina roƙonka, bari
mutumin Allahn da ka aiko mana yă sāke zuwa don yă koya mana yadda za mu
goyi yaron da za a haifa."
9 Allah ya ji Manowa, sai mala'ikan Allah ya sāke zuwa wurin matar yayinda take
gona; amma Manowa mijinta ba ya tare da ita. 10 Sai matar ta ruga don ta faɗa wa
mijinta, ta ce, "Ga shi ya zo! Mutumin da ya bayyana mini ran nan!"
11 Manowa ya tashi ya bi matarsa. Da ya zo wurin mutumin, sai ya ce, "Kai ne
wanda ka yi magana da matata?"
Ya ce, "Ni ne."
12 Saboda haka Manowa ya tambaye shi ya ce, "Sa'ad da maganarka ta cika, me za
tă zama dokar rayuwar yaron da kuma aikinsa?"
13 Mala'ikan Ubangiji ya ce, "Dole matarka ta kiyaye duk abin da na riga na gaya
mata. 14 Kada tă ci kowane iri abin da ya fito daga inabi, ba kuwa za tă sha ruwan
inabi, ko abu mai sa maye ko ta ci abu marar tsarki ba. Dole tă kiyaye duk abin da
na umarce mata."
15 Manowa ya ce wa mala'ikan Ubangiji, "Muna roƙonka ka jira mu yanka maka
ɗan akuya."
16 Mala'ikan Ubangiji ya ce, "Ko kun sa na tsaya, ba zan ci abincinku ba. Amma
in kun shirya hadaya ta ƙonawa, ku miƙa wa Ubangiji." (Manowa bai gane cewa
mala'ikan Ubangiji ne ba.)
17 Sa'an nan Manowa ya sāke tambayi mala'ikan Ubangiji ya ce, "Mene ne sunanka,
don mu girmama ka sa'ad da maganarka ta tabbata."
18 Ya ce, "Me ya sa kake tambaya sunana? Ai, ya wuce fahimta." 19 Sa'an nan
Manowa ya ɗauki ɗan akuya, tare da hadaya ta hatsi ya miƙa wa Ubangiji a kan
dutse. Ubangiji kuwa ya yi abin mamaki yayinda Manowa da matarsa suke kallo.
20 Yayinda harshen wuta ya yi sama daga bagaden, sai mala'ikan Ubangiji ya haura
cikin harshen wutar. Da ganin wannan Manowa da matarsa suka fāɗi da fuskokinsu
har ƙasa. 21 Da mala'ikan Ubangiji bai ƙara bayyana kansa ga Manowa da matarsa
ba, sai Manowa ya gane cewa mala'ikan Ubangiji ne.
22 Ya ce wa matar, "Ba shakka za mu mutu, gama mun ga Allah!"
23 Amma matar ta ce, "Da Ubangiji yana nufin kashe mu ne, da ba zai karɓi hadaya
ta ƙonawa da hadaya ta hatsi daga hannunmu, ko yă nuna mana dukan waɗannan
abubuwa ko abin da ya gaya mana ba."
24 Matar kuwa ta haifi ɗa, aka sa masa suna Samson. Ya yi girma Ubangiji kuma ya
albarkace shi, 25 Ruhun Ubangiji kuwa ya fara iza shi yayinda yake a Mahane Dan,
tsakanin Zora da Eshtawol.

# 14

*Auren Samson*

1 Samson ya gangara zuwa Timna a can ya ga wata daga cikin 'yan mata Filistiyawa.
2 Da ya komo, sai ya gaya wa mahaifinsa da mahaifiyarsa ya ce, "Na ga wata mace a
Timna; ku auro mini ita ta zama matata."
3 Mahaifinsa da mahaifiyarsa suka ce, "Babu wata karɓaɓɓiyar yarinya a cikin
zuriyarku ko cikin dukan mutanenmu ne? Dole ne ka tafi wajen Filistiyawa marasa
kaciya ka nemi aure?"
Amma Samson ya ce wa mahaifinsa, "A auro mini ita dai. Ita ta dace da ni."
4 (Iyayensa ba su san cewa wannan daga wurin Ubangiji ne ba, wanda yake neman
hanyar da za a kai wa Filistiyawa hari; gama a lokacin suna mulkin Isra'ila.)
5 Sai Samson ya gangara zuwa Timna tare da mahaifinsa da kuma mahaifiyarsa.
Da suka yi kusa da gonar inabin Timna, nan da nan sai ga ɗan zaki ya taso ya nufe

shi yana ruri. 6 Ruhun UBANGIJI kuwa ya sauko masa da ƙarfi, ya sa ya yaga zakin
kashi biyu da hannu kamar yadda akan yayyage ɗan akuya. Sai dai bai gaya wa
iyayensa abin da ya yi ba. 7 Sa'an nan ya gangara ya yi magana da yarinyar, yana
kuwa sonsa.
8 Daga baya, da ya koma don yă aure ta, sai ya ratse don yă ga gawar zakin. Sai
ga taron ƙudan zuma da zuma a ciki, 9 wanda ya sa hannu ya ɗebo yana tafiya yana
sha. Sa'ad da ya iso wurin iyayensa, ya ba su zuman, su ma suka sha. Sai dai bai
gaya musu cewa ya ɗebo zuman daga gawar zaki ba.
10 To, mahaifinsa ya gangara don yă ga yarinyar. Samson kuwa ya shirya wata
liyafa a can, yadda yake bisa ga al'adar angwaye. 11 Sa'ad da ya bayyana, sai aka
haɗa shi abokai talatin.
12 Sai Samson ya ce, "Bari in yi muku kacici-kacici, in kun ba ni amsa cikin kwana
bakwai na wannan biki, zan ba ku riguna lilin talatin da kuma tufafi talatin. 13 In
kuma ba ku iya ba ni amsar ba, dole ku ba ni rigunan lilin talatin da tufafi talatin."
Suka ce, "Ka gaya mana kacici-kacicin."
14 Sai ya ce,
"Daga mai ci, abinci ya fito;
daga mai ƙarfi, abu mai zaki ya fito."
Har kwana uku ba su iya ba da amsa ba.
15 A rana ta huɗu* suka ce wa matar Samson "Ki rarrashi mijinki yă bayyana mana
kacici-kacicin, ko kuwa mu ƙone ki da gidan mahaifinki duka da wuta. Kun kira mu
domin ku yi mana fashi ne?"
16 Sa'an nan matar Samson ta kwanta masa a jiki tana kuka tana cewa, "Kai
maƙiyina ne, lalle ba ka ƙaunata, ka yi wa mutanena kacici-kacici, amma ba ka
gaya mini amsar ba."
Ya amsa ya ce, "Ban ma bayyana wa mahaifina ko mahaifiyata ba, to, don me zan
bayyana miki?" 17 Ta yi ta kuka har kwana bakwai na bikin. Saboda haka a rana
ta bakwai sai ya gaya mata, don ta dame shi. Ita kuwa ta bayyana kacici-kacicin wa
mutanenta.
18 Kafin rana ta fāɗi a rana ta bakwai mutane garin suka ce masa,
"Me ya fi zuma zaki?
Me ya fi zaki ƙarfi?"
Samson ya ce musu,
"Da ba don kun haɗa baki da matata ba,
da ba za ku san amsar kacici-kacici ba."
19 Sa'an nan Ruhun UBANGIJI ya sauko masa da iko. Sai ya fita ya gangara zuwa
Ashkelon, ya kashe mutanensu talatin, ya kwashe kayansu ya kuma ba da rigunarsu
ga waɗanda suka bayyana kacici-kacicin. Cike da fushi, ya haura zuwa gidan
mahaifinsa. 20 Aka kuma ɗauki matar Samson aka ba wa ɗaya daga cikin waɗanda
suka yi masa hidima a bikin.

# 15

*Sakayyar Samson a kan Filistiyawa*

1 Daga baya, a lokacin girbin alkama, Samson ya ɗauki ɗan akuya ya tafi yă ziyarci
matarsa. Sai ya ce, "Zan in shiga ɗakin matata." Amma mahaifinta ya hana shi shiga.
2 Ya ce wa, "Na tabbata ba ka sonta sam-sam, don haka na ba da ita ga abokinka.
Ba ƙanuwarta ta fi kyau ba? Ka ɗauke ta a maimako."
3 Samson kuwa ya ce musu, "A wannan lokaci ina da iko in rama a kan Filistiyawa;
tabbatacce zan ji musu." 4 Saboda haka ya tafi ya kama yanyawa ɗari uku ya

* **14:15** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na Seftuwajin da na Siriyak; da na Ibraniyanci suna da bakwai

ɗaura wutsiyoyinsu wutsiya da wutsiya. Sa'an nan ya daure acibalbal a tsakanin
ko waɗanne wutsiya biyu, 5 sai ya sa wa acibalbal wuta, ya saki yanyawan suka
shiga gonakin Filistiyawa. Suka ƙone dammunan hatsi da hatsin da yake tsaye, tare
da gonakin inabi da na zaitun.
6 Filistiyawa suka yi tambaya suka ce, "Wane ne ya yi wannan abu?" Sai aka ce
musu, "Ai, Samson ne surukin mutumin Timna, domin an ba wa abokinsa matarsa."
Saboda haka Filistiyawa suka haura suka je suka ƙone ta da mahaifinta ƙurmus
da wuta. 7 Samson ya ce musu, "Tun da kun aikata wannan, ba zan bari ba har sai
na ɗau fansa a kanku." 8 Ya kuwa fāɗa musu ya kuma karkashe su da yawa. Sa'an
nan ya gangara ya zauna a kogo a dutsen Etam.
9 Filistiyawa suka haura suka yi sansani a Yahuda, suka bazu kusa da Lehi.
10 Mutanen Yahuda suka ce, "Me ya sa kuka zo mana da yaƙi?"
Sai suka ce, "Mun zo ne mu kama Samson, a matsayin fursunan yaƙi, mu yi masa
kamar yadda ya yi mana."
11 Sa'an nan mutane dubu uku daga Yahuda suka gangara wajen Samson a kogo a
dutsen Etam. Suka ce masa, "Ba ka san cewa Filistiyawa ne suke mulkinmu ba? Me
ke nan ka yi mana?"
Ya ce musu, "Na ɗan yi musu abin da suka yi mini ne."
12 Suka ce masa, "To, mun zo ne mu daure ka mu kai wa Filistiyawa."
Samson ya ce, "Ku rantse mini ba za ku kashe ni da kanku ba."
13 Suka ce, "Mun yarda, za mu dai daure ka mu ba da kai gare su. Ba za mu kashe
ka ba." Saboda haka suka daure shi da sababbin igiyoyi biyu, suka saukar da shi daga
dutsen. 14 Yayinda ya zo gab da Lehi, sai Filistiyawa suka sheƙo a guje da ihu suka
nufo shi. Ruhun UBANGIJI kuwa ya sauko da iko a kansa. Igiyoyin da suke daure a
hannuwansa kuwa suka zama kamar abin da wuta ta babbaka, suka tsintsinke suka
zuba daga hannuwansa. 15 Da ya samo muƙamuƙin jaki, ya ɗauka, sai ya karkashe
mutane dubu ɗaya.
16 Sa'an nan Samson ya ce,
"Da muƙamuƙin jaki
na mai da su jakuna.*
Da muƙamuƙin jaki
na kashe mutum dubu."
17 Da ya gama magana, sai ya jefar da muƙamuƙin; aka ba wa wannan wuri suna
Ramat Lehi.†
18 Saboda ƙishirwa ta kama shi ƙwarai, sai ya ce wa UBANGIJI, "Ka ba bawanka
wannan babbar nasara. To, sai in mutu da ƙishirwa, har in shiga a hannun marasa
kaciyan nan su kashe ni?" 19 Sa'an nan Allah ya buɗe wani rami a Lehi, ruwa kuwa
ya fito daga ciki. Da Samson ya sha, sai ƙarfinsa ya dawo, ya kuma wartsake. Aka sa
wa wannan maɓulɓula suna En Hakkore,‡ yana nan a Lehi har wa yau.
20 Samson kuwa ya shugabanci Isra'ila shekara ashirin a zamanin Filistiyawa.

# 16

*Samson da Delila*

1 Wata rana Samson ya tafi Gaza, inda ya ga wata karuwa. Ya shiga wurinta ya
kwana. 2 Aka gaya wa mutanen Gaza, "Ai, Samson yana a nan!" Saboda haka suka
zo suka kewaye wurin suka yi kwanto dukan dare a bakin ƙofar birni. A daren nan
ba su motsa nan da can ba, suna cewa, "Gari yana wayewa za mu kashe shi."

* **15:16** Ko kuwa mai da su tsibi guda ko biyu; Ibraniyanci na kalman nan jaki ya yi kamar ta Ibraniyanci na tsibi. † **15:17** Ramat Lehi yana nufin tudun muƙamuƙi. ‡ **15:19** En Hakkore yana nufin maɓulɓular mai kira.

3 Amma Samson ya yi kwanciyarsa har tsakiyar dare. Sa'an nan ya tashi ya kama
ƙofofin birnin, tare da madogarai biyunsu, ya tumɓuke, ya aza su a kafaɗarsa, ya kai
su kan dutsen da yake a fuskantar Hebron.
4 Bayan ɗan lokaci, sai ya shiga ƙaunar wata mace, mai suna Delila a Kwarin Sorek.
5 Sai shugabannin Filistiyawa suka tafi wurinta suka ce, "Ki yi ƙoƙari ki ga ko za ki
rarrashe shi yă nuna miki asirin ƙarfinsa da yadda za mu iya shan ƙarfinsa don mu
ɗaura shi mu yi nasara a kansa. Kowannenmu zai ba ki shekel dubu ɗari ɗaya na
azurfa."
6 Saboda haka Delila ta ce wa Samson, "Ka faɗa miki asirin ƙarfinka da yadda za
a ɗaura ka a yi nasara a kanka."
7 Samson ya ce mata, "In wani ya ɗaura ni da sababbin igiyoyin* da ba su bushe
ba, zan zama marar ƙarfi kamar kowa."
8 Sa'an nan shugabannin Filistiyawa suka kawo mata sababbin igiyoyi guda bakwai
da ba su bushe ba, sai ta daure shi da su. 9 Da mutane a ɓoye a cikin ɗaki tare da
ita, sai ta yi ihu ta ce, "Samson ga Filistiyawa sun zo su kama ka!" Da jin haka sai ya
tsintsinke igiyoyin kamar zaren da ya yi kusa da harshen wuta. Saboda haka asirin
ƙarfinsa bai tonu ba.
10 Sa'an nan Delila ta ce wa Samson, "Ka mai da ni wawiya; ka ruɗe ni. Yanzu, ka
gaya mini yadda za a daure ka."
11 Ya ce, "In wani ya ɗaura ni sosai da sababbin igiyoyin da ba a taɓa amfani da su
ba, zan zama marar ƙarfi kamar kowa."
12 Saboda haka Delila ta ɗauki sababbin igiyoyi ta ɗaura shi da su. Sa'an nan, tare
da mutane a ɓoye a ɗakin, ta yi ihu ta ce, "Samson ga Filistiyawa sun zo su kama
ka!" Amma sai ya tsintsinke su kamar zare.
13 Sa'an nan Delila ta ce, "Har yanzu, ka mai da shashasha, kana mai da ni wawiya
kana kuma yin mini ƙarya. Ka gaya mini yadda za a daure ka mana."
Ya ce mata, "In kin yi kitson gashin kaina guda bakwai kika ɗaura su da zare kika
buga su da akwasha, zan rasa ƙarfi in zama kamar kowa." Saboda haka yayinda
yake barci, sai Delila ta yi kitson gashin kansa guda bakwai ta ɗinka su da zare, 14 ta
kuma† ɗaura su da akwasha.
Ta sāke yin ihu ta ce, "Samson ga Filistiyawa sun zo su kama ka." Ya tashi daga
barcinsa ya tumɓuke akwashan tare da zaren da aka ɗaura gashin kansa da su.
15 Sa'an nan ta ce masa, "Yaya kake cewa kana sona alhali ba ka yarda da ni ba?
Wannan shi ne sau na uku kana mai da ni wawiya kuma ba ka nuna mini asirin
ƙarfinka ba." 16 Da irin wannan fitina ta tsokane shi kwana da kwanaki har sai da
ya gaji kamar zai mutu.
17 Saboda haka sai ya faɗa mata kome ya ce, "Ba a taɓa sa reza a kaina ba, domin
ni Naziri ne keɓaɓɓe ga Allah tun haihuwa. In kuwa an aske kaina, ƙarfina zai rabu
da ni, sai in zama kamar kowa."
18 Da Delila ta gane ya gaya mata kome yanzu, sai ta aika saƙo zuwa ga shugabannin
Filistiyawa ta ce, "Ku ƙara zuwa sau ɗayan nan, ai, ya gaya mini kome." Saboda haka
shugabannin Filistiyawa suka dawo tare da azurfa a hannuwansu. 19 Bayan ta sa shi
ya yi barci a cinyarta, sai ta kira wani ya zo ya aske kitso guda bakwai nan a kansa,
aka fara rinjayensa. Karfinsa kuwa ya rabu da shi.
20 Sa'an nan ta yi ihu ta ce, "Samson ga Filistiyawa sun zo su kama ka!"
Sai ya farka daga barci yana tsammani cewa, "Zan fita kamar dā in miƙe jikina."
Amma bai san cewa UBANGIJI ya rabu da shi ba.

* **16:7** Ko kuwa igiyar baka; haka ma a ayoyi 8 da 9. † **16:14** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na Seftuwajin; Ibraniyanci "Zan iya idan kin yi kitson gashin kaina guda bakwai su zama zare a daure." 14 Saboda haka ta

21 Sa'an nan Filistiyawa suka fizge shi, suka ƙwaƙule idanunsa suka gangara da
shi zuwa Gaza. Da suka daure shi da sarƙoƙin tagulla, sai aka sa shi yana niƙa a
kurkuku. 22 Amma gashi kansa ya fara tohuwa kuma bayan an aske shi.
23 To, sai Filistiyawa suka taru don su miƙa hadaya ga Dagon allahnsu su kuma yi
biki cewa, "Allahnmu ya bashe abokin gābanmu Samson a hannuwanmu."
24 Sa'ad da mutane suka gan shi, sai suka yabi allahnsu, suna cewa,
"Allahnmu ya bashe abokin gābanmu
a hannunmu,
wanda ya lalace ƙasarmu
ya kuma raɓanya kisan mutanenmu."
25 Yayinda suke cikin farin ciki, sai suka yi ihu, suka ce, "Fito mana da Samson yă
yi mana wasa." Saboda haka aka zo da Samson daga kurkuku, shi kuwa ya yi wasa
a gabansu.
Sa'ad da suka tsai da shi a tsakanin ginshiƙai, 26 sai Samson ya ce wa bawan da
ya riƙe hannunsa, "Ka kai ni inda zan taɓa ginshiƙan da suke ɗauke da wannan
haikali, don in jingina a kai." 27 To, haikalin ya cika da mutane maza da mata; dukan
shugabannin Filistiyawa kuwa suna a can, a bisan rufin kuwa akwai mutum wajen
dubu uku maza da mata suna kallon Samson yana wasa. 28 Sa'an nan Samson ya
yi addu'a ga UBANGIJI ya ce, "Ya UBANGIJI Mai Iko Duka, ya Allah ka tuna da ni, ka
ƙarfafa ni sau ɗaya nan kaɗai, ka bar ni da bugu ɗaya kawai in ɗauki fansa a kan
Filistiyawa domin idanuna." 29 Sa'an nan Samson ya kai hannuwansa ga ginshiƙan
waɗanda haikalin yake a kai, ya jingina jikinsa, hannunsa dama yana a ɗaya, hannun
hagu kuma na ɗayan, 30 Samson ya ce, "Bari in mutu tare da Filistiyawa!" Sa'an nan
da dukan ƙarfinsa ya tura haikali ya fāɗa a kan shugabanni da dukan mutanen da
suke ciki. Ta haka ya kashe mutane da yawa fiye da yayinda yake da rai.
31 Sa'an nan 'yan'uwansa da dukan dangin mahaifinsa suka gangaro don su ɗauke
shi. Suka kawo shi suka binne tsakanin Zora da Eshtawol a kabarin Manowa
mahaifinsa. Ya yi mulkin Isra'ila shekara ashirin.

# 17

*Gumakan Mika*
1 To, wani mutum mai suna Mika daga ƙasar tudu ta Efraim 2 ya ce wa mahaifiyarsa,
"Shekel dubu ɗaya da ɗari ɗaya na azurfa da aka ɗauka daga gare ki wanda kuma
ji kin furta la'ana a kai, azurfan yana wurina; ni ne na ɗauka."
Sa'an nan mahaifiyarsa ta ce, "UBANGIJI yă albarkace ka ɗana!"
3 Sa'ad da ya mayar da azurfa dubu ɗaya da ɗari ɗaya na shekel wa mahaifiyarsa,
sai ta ce, "Na ba da azurfata ga UBANGIJI don ɗana yă sassaƙa sura yă kuma yi zubin
gunki. Zan mayar maka."
4 Saboda haka ya mayar da azurfan wa mahaifiyarsa, ita kuwa ta ɗauki azurfa ɗari
biyu na shekel ta ba wa maƙeri, wanda ya mai da su sura da kuma gunki. Aka kuwa
sa su a gidan Mika.
5 To, wannan mutum Mika yana da ɗakin gumaka, ya yi efod da waɗansu gumaka,
ya kuma naɗa ɗaya daga cikin 'ya'yansa firist nasa. 6 A kwanakin Isra'ila ba ta da
sarki; kowa yana yin abin da ya ga dama.
7 Wani saurayi Balawe daga Betlehem a Yahuda, wanda yake zama cikin zuriyar
Yahuda, 8 ya bar garin ya tafi neman inda zai zauna. A hanyarsa* ya zo gidan Mika
a ƙasar tudu ta Efraim.
9 Mika ya ce masa, "Daga ina kake?"
Ya ce, "Ni Balawe ne daga Betlehem a Yahuda, ina kuwa neman wurin zauna ne."

* 17:8 Ko kuwa Don yin sana'arsa

10 Sa'an nan Mika ya ce masa, “Ka zauna tare da ni ka zama mini mahaifi da firist,
zan kuwa ba ka azurfa goma na shekel a shekara, tufafinka da kuma abincinka.” Sai
Balawen ya tafi. 11 Saboda haka Balawen ya yarda ya zauna tare da shi, ɗan saurayin
kuwa ya zama kamar ɗaya daga cikin 'ya'yansa. 12 Sa'an nan Mika ya naɗa Balawen,
saurayin kuwa ya zama masa firist ya kuma zauna a gidansa. 13 Mika ya ce, “Yanzu
na san cewa Ubangiji zai yi mini alheri, da yake Balawen nan ya zama firist nawa.”

# 18

*Mutanen Dan sun zauna a Layish*

1 To, a kwanakin nan Isra'ila ba ta da sarki.
A kwanakin kuwa zuriyar Dan tana neman wurinsu na zama, gama ba su riga
sun sami gādo tare da kabilan Isra'ila ba. 2 Saboda haka mutanen Dan suka aika
jarumawa guda biyar daga Zora da Eshtawol don su leƙi asirin ƙasar su kuma bincike
ta. Waɗannan mutanen sun wakilci dukan kabilar. Suka ce musu, “Ku je, ku bincike
ƙasar.”
Mutanen suka shiga ƙasar tudu ta Efraim suka zo gidan Mika, inda suka kwana.
3 Sa'ad da suka yi kusa da gidan Mika, sai suka gane muryar saurayin nan Balawe;
saboda haka suka shiga wurin suka tambaye shi, “Wa ya kawo ka nan? Me kake yi a
nan? Me ya sa kake a nan?”
4 Ya gaya musu abin da Mika ya faɗa masa ya ce, “Ya ɗauke ni aiki ya kuma sa in
zama masa firist.”
5 Sa'an nan suka ce masa, “Muna roƙonka ka nemi mana nufin Allah don mu sani
ko tafiyarmu tana da nasara.”
6 Firist ya amsa ya ce, “Ku sauka lafiya, gama tafiyarku tana da yardan Ubangiji.”
7 Saboda haka mutum biyar ɗin suka tashi suka iso Layish, inda suka ga mutane
suna zamansu a huce, kamar Sidoniyawa, ba sa zato ga tsaro. Kuma da yake ƙasarsu
ba ta bukata kome, suna da wadata. Suna kuma nesa da Sidoniyawa, ba sa kuma
hulɗa da kowa.
8 Da suka komo Zora da Eshtawol, 'yan'uwansu suka tambaye su, “Me kuka gano?”
9 Suka ce, “Ku zo mu yaƙe su! Mun ga ƙasar tana da kyau sosai. Ba za ku yi wani
abu ba? Kada ku yi wata-wata, ku je kun mallaki ƙasar. 10 Sa'ad da kun kai can,
za ku iske mutanen suna zama a sake, ƙasar kuwa mai faɗi ce wadda Allah ya sa a
hannuwanku, ƙasar da ba tă rasa kome ba.”
11 Sai mutane ɗari shida daga kabilar Dan suka yi ɗamarar yaƙi, suka tashi daga
Zora da Eshtawol. 12 A kan hanyarsu suka kafa sansani kusa da Kiriyat Yeyarim a
Yahuda. Shi ya sa a ana kira wurin nan yamma da Kiriyat Yeyarim Mahane Dan* har
wa yau. 13 Daga can suka tafi ƙasar tudu ta Efraim suka zo gidan Mika.
14 Sa'an nan mutum biyar ɗin nan da suka leƙi asirin ƙasar Layish suka ce wa
'yan'uwansu, “Kun san cewa ɗaya daga cikin gidajen nan yana da efod, waɗansu
allolin iyali, siffar da aka sassaƙa da kuma gunki na zubi? To, kun san abin da za
ku yi.” 15 Saboda haka suka juya a wurin suka shiga gidan saurayin nan Balawe a
wajen Mika suka gaishe shi. 16 Mutanen Dan ɗari shida da suka sha ɗamarar yaƙi
suka tsaya a bakin ƙofa. 17 Sai mutum biyar da suka leƙi asirin ƙasar suka shiga ciki
suka ɗauke gunkin da aka sassaƙa, efod, sauran allolin gida da kuma gunki na zubi
yayinda firist ɗin tare da mutane ɗari shida da suka yi ɗamarar yaƙi suna tsaye a
bakin ƙofa.
18 Sa'ad da waɗannan mutane suka shiga gidan Mika suka ɗauke gunkin da aka
sassaƙa, efod, sauran allolin gida da kuma gunki na zubi, sai firist ya ce musu, “Me
kuke yi?”

* **18:12** Mahane Dan yana nufin Sansanin Dan.

19 Suka ce, “Ka yi shiru! Kada ka ce wani abu. Zo tare da mu, ka zama mahaifinmu
da kuma firist. Bai fi maka ka yi wa kabila da kuma zuriya a Isra’ila aikin firist ba,
da ka bauta wa iyali guda kawai?” 20 Sai firist ya yi farin ciki. Ya ɗauki efod, sauran
allolin gida da siffar da aka sassaƙa ya tafi tare da mutanen. 21 Suka sa ’ya’yansu
ƙanana a gaba, dabbobinsu da mallakansu a gabansu, suka juya suka tafi.
22 Sa’ad da suka yi ɗan nisa daga gidan Mika, sai aka kira mutanen da suke
maƙwabtakar da Mika suka taru suka bi mutanen Dan suka cim musu. 23 Da suna
ihu suna binsu, sai mutanen Dan suka waiga suka cewa Mika, “Mece ce damuwarka
da ka kira mutanenka su zo su fāɗa mana?”
24 Ya amsa ya ce, “Kun kwashe allolin da na yi, da kuma firist nawa, kuka tafi. Me
kuma nake da shi? Yaya za ku ce, ‘Mece ce damuwata?’ ”
25 Mutanen Dan suka ce, “Kada ka kuskura ka ce kome, in ba haka ba mutanen nan
za su harzuƙa, da kai da iyalinka duka ku rasa rayukanku.” 26 Saboda haka mutanen
Dan suka kama hanyarsu, Mika kuwa da ya ga an fi ƙarfinsa, sai ya juya ya koma
gida.
27 Sa’an nan suka ɗauko abin da Mika ya yi, da firist nasa, suka tafi Layish, suka
fāɗa wa mutanen da suke zaman lafiya, ransu kuma a kwance. Suka fāɗa musu suka
kuma ƙone birninsu. 28 Ba wanda zai cece su domin suna nesa da Bet-Sidon kuma
ba sa hulɗa da kowa. Birnin yana a kwari kusa da Bet-Rekob.
Mutanen Dan suka sāke gina birnin suka zauna a can. 29 Suka sa wa birnin suna
Dan, wato, sunan kakansu Dan, wanda aka haifa wa Isra’ila, ko da yake a dā ana
kira birnin Layish. 30 A can mutanen Dan suka kafa wa kansu gumaka, Yonatan ɗan
Gershom, ɗan Musa,† da ’ya’yansa maza firistoci ne na kabilar Dan har lokacin da
aka kwashe mutane zuwa bauta. 31 Suka ci gaba da amfani da gumakan da Mika ya
yi, a duk wannan lokacin gidan Allah yana a Shilo.

# 19

*Balawe da ƙwarƙwarasa*

1 A kwanakin nan Isra’ila ba su da sarki.
To, wani Balawe wanda yake zama a wani lungu na ƙasar tudu ta Efraim ya ɗauko
wa kansa ƙwarƙwara daga Betlehem cikin Yahuda. 2 Amma ba tă yi aminci ba. Ta
bar shi ta komo gidan mahaifiyarta a Betlehem, a Yahuda. Bayan ta zauna a can
wajen wata huɗu, 3 sai mijinta ya je wajenta biko don yă rarashe ta komo. Ya tafi
tare bawansa da kuma jakuna biyu. Sai ta shigar da shi gidan mahaifinta, sa’ad da
mahaifinta ya gan shi, ya marabce shi da murna. 4 Surukinsa, mahaifin yarinyar, ya
sha kansa, yă dakata; saboda haka ya dakata tare da shi har kwana uku, yana ci yana
sha, yana kuma kwanciya a can.
5 A rana ta huɗu suka tashi da sassafe ya kuma yi shiri yă tafi, amma mahaifinta
yarinyar ya ce wa surukinsa, “Ka ɗan ci wani abu don ka sami ƙarfi; sa’an nan
ka tafi.” 6 Saboda haka suka zauna su biyu suka ci suka sha tare. Bayan haka sai
mahaifin yarinyar ya ce, “Don Allah ka kwana ka ji wa kanka daɗi.” 7 Sa’ad da
mutumin ya tashi zai tafi, sai surukinsa ya roƙe shi, saboda haka ya kwana a wannan
dare. 8 Da sassafen kashegari rana ta biyar, ya tashi zai tafi, sai mahaifin yarinyar ya
ce, “Ka ɗan zauna ka shaƙata sai rana ta yi sanyi mana!” Saboda haka su biyu suka
zauna suka ci abinci tare.
9 Sa’ad da mutumin da ƙwarƙwaransa da bawansa, suka tashi don su tafi,
surukinsa, mahaifin yarinyar ya ce, “Duba, rana ta kusan fāɗuwa, yamma ta riga
ta yi, ka kwana a nan. Ka sāke kwana ka ji wa ranka daɗi. Kashegari da sassafe za
ka iya tashi ka kama hanyarka zuwa gida.” 10 Amma bai so ya sāke kwana a can ba,

† **18:30** Rubutun al’adu na dā na Ibraniyanci, da waɗansu rubuce-rubucen hannun Seftuwajin da na Bulget; da Nassin Masoretik Manasse

mutumin ya tashi ya tafi ya bi ta Yebus (wato, Urushalima), tare da jakunansa biyu da aka yi musu shimfiɗa da kuma ƙwarƙwaransa.
11 Sa'ad da suka yi kusa da Yebus dare kuma ya riga ya yi, bawan ya ce wa maigidansa, "Mu dakata a birnin nan na Yebusiyawa mu kwana."
12 Maigidansa ya ce, "A'a. Ba za mu shiga birnin baƙi waɗanda mutanensu ba Isra'ilawa ba. Za mu ci gaba zuwa Gibeya." 13 Ya kuma ce, "Zo, mu yi ƙoƙari mu kai
Gibeya ko Rama mu kwana a ɗaya cikinsu." 14 Saboda haka suka ci gaba, rana tana
fāɗuwa sa'ad da suka yi kusa da Gibeya a Benyamin. 15 A can suka dakata don su
kwana, suka tafi suka zauna a dandali birnin, amma wani ya shigar da su gidansa da daren.
16 A wannan yamma sai ga wani tsoho daga ƙasar tudu ta Efraim, wanda yake zama a Gibeya (mutane wurin kuwa mutanen Benyamin ne), ya shigo daga wurin aiki a gonaki. 17 Sa'ad da ya duba ya ga matafiyin a dandalin birnin, sai tsohon ya yi tambaya ya ce, "Ina za ku? Ina kuka fito?"
18 Balawen ya ce, "Muna fito daga Betlehem a Yahuda za mu wani lungu a ƙasar tudu ta Efraim inda nake da zama. Na tafi Betlehem a Yahuda, ga shi kuwa yanzu za ni gidan UBANGIJI. Ba wanda ya shigar da ni gidansa. 19 Muna da ƙara da abinci
don jakunanmu, muna kuma da burodi da ruwan inabi dominmu da bayinka, ni, baiwarka da kuma saurayin nan tare da mu. Ba ma bukatar kome."
20 Tsohon ya ce, "Na marabce ku a gidana. Bari ni ba ku duk abin da kuke bukata. Kada ku dai kwana a dandali." 21 Saboda haka sai kai shi zuwa gidansa ya ciyar da jakunansa. Bayan sun wanke ƙafafunsu, sai aka ba su abinci da abin sha.
22 Yayinda suke jin wa kansu daɗi, sai waɗansu 'yan iska daga birnin suka kewaye gidan. Suna bubbuga ƙofar, suna kira tsohon da yake da gidan suna cewa, "Ka fito mana da mutumin nan a gidanka domin mu yi jima'i da shi."
23 Maigidan ya fita waje ya ce musu, "A'a, abokaina, kada ku yi abin kunyan nan. Da yake mutumin nan baƙona ne, kada ku yi rashin kunyan nan. 24 Duba, ga 'yata
da ba tă taɓa sanin namiji ba da kuma ƙwarƙwaransa. Zan fito muku da su a waje yanzu, za ku kuwa iya yin ko mene ne da kuke so da su. Amma wannan mutum, kada ku yi abin kunya."
25 Amma mutanen ba su saurare shi ba. Saboda haka mutumin ya ba da ƙwarƙwaransa, suka yi mata fyaɗe suka yi lalata da ita dukan dare, gari yana
wayewa sai suka bar ta. 26 Da safe matar ta koma gidan da maigidanta yake, ta fāɗi a ƙofa ta kwanta a can har rana ta yi.
27 Sa'ad da maigidanta ya tashi da safe ya buɗe ƙofar gidan don yă fita ya ci gaba da tafiyarsa, sai ga ƙwarƙwararsa, ta fāɗi a bakin ƙofar gidan da hannuwanta a
madogarar ƙofar. 28 Ya ce mata, "Tashi; mu tafi." Amma ba amsa. Sai ya sa ta a kan jakinsa ya kama hanyar gida.
29 Da ya kai gida, sai ya ɗauki wuƙa ya yayyanka ƙwarƙwaransa gunduwa-gunduwa, kashi goma sha biyu ya aika da su a ko'ina a Isra'ila. 30 Duk wanda ya
gani, sai ya ce, "Ba a taɓa gani ko yin irin wannan abu ba, tun lokacin da Isra'ilawa suka fito daga Masar. Ku yi tunani wannan! Ku kuma yi la'akari! Ku gaya mana abin da za mu yi!"

# 20

*Isra'ila sun yaƙi mutanen Benyamin*

1 Sa'an nan dukan Isra'ilawa daga Dan zuwa Beyersheba kuma daga ƙasar
Gileyad mutane kamar mutum guda suka fito suka taru a gaban UBANGIJI a Mizfa.
2 Shugabanni dukan kabilan mutane na kabilan Isra'ila suka zazzauna a wurarensu
a taron jama'ar Allah, mayaƙa dubu ɗari huɗu masu ɗamara da takuba. 3 (Mutanen

Benyamin suka ji cewa Isra'ilawa sun haura zuwa Mizfa.) Sa'an nan Isra'ilawa suka
ce, “Gaya mana yadda wannan mugun abu ya faru.”
4 Sai Balawen, mijin matar da aka kashe ya ce, “Ni da ƙwarƙwarata mun zo Gibeya
a Benyamin don mu kwana. 5 Da dad dare mutanen Gibeya suka bi ni suka kewaye
gidan da niyya su kashe ni. Suka yi wa ƙwarƙwarata fyaɗe, har ta mutu. 6 Na ɗauki
ƙwarƙwarata na yayyanka gunduwa-gunduwa na aika da shi ga kowane yankin
gādon Isra'ila, domin sun aikata mugu abu da abin kunya a Isra'ila. 7 To, dukanku
Isra'ilawa, sai ku yi magana ku kuma yanke hukuncinku.”
8 Dukan mutane suka tashi kamar mutum ɗaya, suna cewa “Ba waninmu da zai tafi
gida. Sam, babu ko ɗayanmu da zai koma gidansa. 9 Amma yanzu ga abin da za mu
yi wa Gibeya. Za mu haura mu fāɗa yadda ƙuri'a ta nunar. 10 Za mu ɗauko mutum
goma a kowane mutum ɗari daga dukan kabilan Isra'ila, da ɗari a dubu, da kuma
dubu a dubu goma, domin a tanada wa mayaƙan. Sa'an nan, sa'ad da mayaƙan suka
iso Geba a Benyamin, za su yi da su daidai bisa ga muguntar da suka yi a Isra'ila.”
11 Saboda haka dukan mutane Isra'ilawa suka taru suka kuma haɗu kamar mutum
guda don su fāɗa wa birnin da yaƙi.
12 Kabilan Isra'ila suka aika jakadu a ko'ina a cikin kabilar Benyamin cewa, “Wace
irin mugunta ce wannan da kuka aikata? 13 Yanzu fa sai ku fitar da waɗannan 'yan
iskan da suka aikata wannan abu na Gibeya don mu kashe su mu kawar da mugunta
daga Isra'ila!”
Amma mutanen Benyamin ba su saurari 'yan'uwansu Isra'ilawa ba. 14 Daga
biranensu suka tattaru a Gibeya don su yaƙi Isra'ilawa. 15 Nan da nan mutanen
Benyamin suka tattara mayaƙa dubu ashirin da shida masu takuba daga biranensu,
ban da mayaƙa ɗari bakwai da aka zaɓa daga mazauna a Gibeya. 16 Cikin dukan
mayaƙan nan akwai zaɓaɓɓu mutane ɗari bakwai waɗanda su bahagwai ne,
kowanne yana iya harbin gashin guda na kai da majajjawa ba kuskure.
17 Isra'ila kuwa, ban da Benyamin, sun tara mayaƙa masu takobi dubu ɗari huɗu,
dukansu gwanayen yaƙi ne.
18 Sai Isra'ilawa suka haura zuwa Betel* suka nemi nufin Allah, suka ce, “Wane ne
a cikinmu zai fara fāɗa wa mutanen Benyamin?”
UBANGIJI ya ce, “Yahuda ce za tă fara.”
19 Kashegari sai Isra'ilawa suka tashi suka kafa sansani kusa da Gibeya. 20 Mutanen
Isra'ila suka fita yaƙi da mutane Benyamin suka kuma ja dāgār yaƙi a Gibeya.
21 Mutanen Benyamin suka fito daga Gibeya suka kashe mutum dubu ashirin da biyu
na Isra'ilawa a dāgār yaƙi a ranar. 22 Amma mutanen Isra'ila suka ƙarfafa juna, suka
sāke koma inda suka ja dāgā a rana ta farko. 23 Isra'ilawa suka haura suka yi kuka
a gaban UBANGIJI, har yamma, suka nemi nufin UBANGIJI. Suka ce, “Mu sāke koma
yaƙi da mutanen Benyamin, 'yan'uwanmu?”
UBANGIJI ya ce, “Ku haura ku fāɗa musu.”
24 Sai Isra'ilawa suka matsa kusa da Benyamin a rana ta biyu. 25 A wannan lokaci,
da mutanen Benyamin suka fito daga Gibeya don su yaƙe su, sai suka sāke kashe
Isra'ilawa dubu goma sha takwas, dukansu ɗauke da takuba.
26 Sa'an nan Isra'ilawa, dukan mutane, suka haura zuwa Betel, a can suka zauna
suna kuka a gaban UBANGIJI. Suka yi azumi a wannan rana har yamma suka miƙa
hadayun ƙonawa da hadayun salama ga UBANGIJI. 27 Isra'ilawa suka nemi nufin
UBANGIJI (A kwanakin nan akwatin alkawarin Allah yana can, 28 Finehas ɗan Eleyazar,
ɗan Haruna, kuwa yana hidima a gabansa.) Suka ce, “Mu sāke haura mu yi yaƙi da
mutanen Benyamin 'yan'uwanmu, ko a'a?”
UBANGIJI ya ce, “Ku je, gama gobe zan ba da su a hannuwanku.”

* **20:18** Ko kuwa zuwa gidan Allah; haka ma a aya 26.

29 Sa’an nan Isra’ila ta yi kwanto kewaya da Gibeya. 30 Suka haura su kara da
mutanen Benyamin a rana ta uku suka ja dāgā a Gibeya kamar dā. 31 Mutanen
Benyamin suka fito su same su aka kuma jawo su nesa da birnin. Suka fara karkashe
Isra’ilawa kamar dā, har aka kashe wajen mutum talatin a filaye da kuma a hanyoyi,
wadda take zuwa Betel da kuma wadda take zuwa Gibeya. 32 Yayinda mutanen
Benyamin suna cewa, “Muna cin nasara a kansu kamar dā,” Isra’ilawa kuwa suna
cewa, “Mu yi ta jan da baya mu janye su daga birni zuwa kan hanyoyi.”
33 Dukan mutanen Isra’ila suka taso daga wurarensu suka ja dāgā a Ba’al-Tamar,
Isra’ilawan da suka yi kwanto a yammancin Geba kuwa suka fito. 34 Sa’an nan
jarumai Isra’ila dubu goma suka yi gaba suka kai wa Gibeya hari. Yaƙi kuwa ya
yi zafi har mutane Benyamin ba su san masifa tana dab da su ba. 35 UBANGIJI
kuwa ya fatattake mutanen Benyamin a gaban Isra’ila; a ranar kuwa Isra’ilawa sun
kashe mutum 25,100 na mutanen Benyamin, dukansu ɗauke da takuba. 36 Sa’an nan
Benyamin suka ga an ci su.
To, mutanen Isra’ila sun yi ta ja da baya daga mutanen Benyamin domin suna
dogara ga waɗanda sa su yi kwanto kusa da Gibeya ne. 37 Mutanen da suke kwanto
suka yi wuf suka ruga cikin Gibeya, suka bazu suka kuma karkashe dukan waɗanda
suke a birnin. 38 Mutanen Isra’ila sun riga sun shirya da ’yan kwanton cewa su
murtuke hayaƙi daga birnin, 39 a sa’an nan ne mutanen Isra’ila za su juya su fāɗa
wa mutane Benyamin da yaƙi.
Mutanen Benyamin sun fara karkashe mutum talatin na Isra’ila, sai suka ce, “Muna
cin nasara a kansu kamar dā.” 40 Amma da alamar hayaƙi ya fara murtukewa daga
birnin, sai mutanen Benyamin suka juya suka ga hayaƙi yana murtukewa ko’ina
a cikin birnin zuwa sararin sama. 41 Sa’an nan mutanen Isra’ila suka juyo musu,
mutanen Benyamin kuwa suka tsorata domin sun gane masifa ta zo musu. 42 Saboda
haka suka tsere a gaban Isra’ila zuwa wajen hamada, amma ba su iya tsere wa
yaƙin ba. Mutanen Isra’ila da suka fito daga cikin birnin suka karkashe su a can.
43 Suka kewaye mutanen Benyamin, suka kore su, suka fatattake su a wajajen Gibeya a
gabashi. 44 Mutum dubu goma sha takwas na mutanen Benyamin suka mutu dukansu
kuwa jarumai ne. 45 Da suka juya suka juya suka tsere zuwa wajajen hamada zuwa
dutsen Rimmon, Isra’ilawa suka kashe mutum dubu biyar a kan hanyoyi. Suka yi ta
matsa wa mutanen Benyamin har zuwa Gidom suka kashe mutum dubu biyu kuma.
46 A ranar kuwa mutanen Benyamin dubu ashirin da biyar ne aka kashe, dukansu
jarumai. 47 Amma mutane ɗari shida suka juya suka tsere wajajen hamada zuwa
dutsen Rimmon, inda suka zauna wata huɗu. 48 Mutanen Isra’ila suka koma wurin
mutanen Benyamin suka kashe dukan waɗanda suke a birnin, tare da dabbobi da
kome da suka samu. Dukan garuruwan da suka samu sun ƙone su ƙaf.

# 21

*Mata don mutanen Benyamin*

1 Mutanen Isra’ila sun riga sun yi rantsuwa a Mizfa cewa, “Ba ɗayanmu da zai ba
da ’yarsa aure ga mutumin Benyamin.”

2 Sai mutanen suka tafi Betel,* inda suka zauna a gaban Allah har yamma, suna
tā da muryoyinsu suna kuka mai zafi. 3 Suka ce, ya UBANGIJI, Allah na Isra’ila, “Me
ya sa wannan abu ya faru da Isra’ila? Don me kabila ɗaya daga Isra’ila za tă ɓace a
yau?”

4 Kashegari da sassafe mutane suka gina bagade suka miƙa hadaya ta ƙonawa da
hadaya ta salama.

* **21:2** Ko kuwa zuwa gidan Allah

5 Sa’an nan Isra’ilawa suka ce, “Wace kabila ce cikin kabilan Isra’ila ba tă zo taro
a gaban UBANGIJI ba?” Gama an yi rantsuwa cewa duk wanda ya kāsa zuwa taro a
gaban UBANGIJI a Mizfa lalle a kashe shi.
6 To, Isra’ilawa suka yi juyayin ’yan’uwansu, mutanen Benyamin. “Yau an hallaka
kabila daga cikin Isra’ila. 7 Yaya za mu ba wa waɗanda suka rage mata, da yake mun
riga mun yi rantsuwa a gaban UBANGIJI, ba za mu ba su ɗaya daga ’ya’yanmu su aura
ba?” 8 Sa’an nan suka ce, “Wace kabila ce cikin kabilan Isra’ila ba tă zo taro a gaban
UBANGIJI a Mizfa ba?” Sai su gane cewa babu wani daga Yabesh Gileyad da ya zo
sansani don taron. 9 Gama da aka yi ƙidaya mutane, sai aka gane cewa babu wani
daga mutanen Yabesh Gileyad da yake a can.
10 Saboda haka sai taron ya umarci jarumai dubu goma sha biyu su je Yabesh
Gileyad su karkashe waɗanda suke zaune a can, duk da mata da yara. 11 Suka ce
musu, “Ga abin da za ku yi. Ku karkashe duk namiji da kowace macen da ta riga
ta san namiji.” 12 Suka samu a cikin mutanen da suke zaune a Yabesh Gileyad mata
ɗari huɗu da ba su taɓa kwana da namiji ba, suka kwashe su zuwa sansani a Shilo
a Kan’ana.
13 Sa’an nan dukan taro suka aika wa mutanen Benyamin da suke a Dutsen Rimmon
cewa yaƙi ya ƙare, yanzu sai salama. 14 Saboda haka mutanen Benyamin suka komo
a lokacin aka kuma ba su matan Yabesh Gileyad nan da aka bari da rai. Amma matan
ba su ishe su duka ba.
15 Mutanen kuwa suka yi juyayi saboda mutanen Benyamin, domin UBANGIJI ya yi
gibi a cikin kabilan Isra’ila. 16 Shugabannin taron suka ce, “Da matan Benyamin da
aka hallaka, yaya za mu yi da mazan da suka ragu da ba su sami mata ba?” 17 Suka
ce, “Dole mutanen Benyamin da suka ragu su sami gādo, domin kada wata kabila a
Isra’ila ta ɓace. 18 Ba za mu iya ba su ’yan matanmu su zama matansu ba, da yake
mu Isra’ilawa mun riga mun yi wannan rantsuwa cewa, ‘La’ananne ne wanda ya ba
da ’yarsa aure ga mutum Benyamin.’ 19 Sai suka tuna, akwai bikin UBANGIJI da sukan
yi shekara-shekara a Shilo ya yi kusa. Shilo yana arewancin Betel, kudu da Lebona,
gabas da hanyar da take tsakanin Betel da Shekem.”
20 Saboda haka suka cewa mutanen Benyamin, “Ku je ku ɓuya a gonakin inabi 21 ku
lura. Sa’ad da ’yan matan Shilo suka fito waje don su yi rawa, ku fito a guje daga
gonakin inabi, kowannenku yă kama wa kansa mata daga cikin ’yan matan Shilo, ku
tafi ƙasar Benyamin. 22 Sa’ad da iyayensu maza ko ’yan’uwansu suka kawo mana
ƙara, za mu ce musu, ‘Ku yi mana alheri ku bar su, domin ba mu samo musu mata
ba lokacin yaƙi, ku kuma marasa laifi ne, tun da yake ba ku ba da ’ya’yan matanku
gare su ba.’ ”
23 Haka mutanen Benyamin suka yi. Yayinda ’yan matan suke rawa, kowane
mutum ya kama ɗaya ya yi gaba da ita ta zama matarsa. Sa’an nan suka komo
ƙasar gādonsu suka sāke giggina garuruwan suka kuwa zauna a cikinsu.
24 A lokacin, Isra’ilawa sun bar wurin suka tafi gida zuwa ga kabilansu da
zuriyoyinsu, kowane zuwa gādonsa.
25 A kwanakin Isra’ila ba ta da sarki; kowa ya yi abin da ya ga dama.

# Rut

*Na'omi ta rasa mijinta da 'ya'yanta maza*
1 A kwanakin da mahukunta suke mulki[*] an yi yunwa a ƙasar, sai wani mutum
daga Betlehem a Yahuda tare da matarsa da 'ya'yansu maza biyu, suka tafi su yi
zama na ɗan lokaci a ƙasar Mowab. 2 Sunan mutumin, Elimelek ne, sunan matarsa
Na'omi; sunayen 'ya'yan nan nasu biyu, su ne Malon da Kiliyon. Su Efratawa ne daga
Betlehem ta Yahuda. Suka kuwa tafi Mowab suka zauna a can.
3 To, Elimelek mijin Na'omi ya rasu, aka bar ta da 'ya'yanta maza biyu. 4 Suka auri
mata Mowabawa, sunan ɗaya Orfa ɗayan kuma Rut. Bayan sun zauna a can kamar
shekara goma, 5 sai Malon da Kiliyon suka mutu su ma, aka kuma bar Na'omi babu
'ya'yanta maza biyu da kuma mijinta.

*Na'omi da Rut sun dawo Betlehem*
6 Sa'ad da ta ji a Mowab cewa UBANGIJI ya zo don yǎ taimaki mutanensa ta wurin
tanada musu da abinci, sai Na'omi tare da surukanta suka shirya su koma gida daga
can. 7 Tare da surukanta biyu suka bar inda suka zauna suka kuma kama hanya da
za tǎ komar da su zuwa ƙasar Yahuda.
8 Sai Na'omi ta ce wa surukanta biyu, "Ku koma, kowannenku, zuwa gidan
mahaifiyarta. Bari UBANGIJI yǎ nuna muku alheri yadda kuka nuna wa matattun
nan da kuma gare ni. 9 Bari UBANGIJI yǎ sa kowannenku ta sami hutu a gidan wani
miji."
Sa'an nan ta sumbace su suka kuma yi kuka da ƙarfi 10 suka ce mata, "Za mu tafi
tare da ke zuwa ga mutanenki."
11 Amma Na'omi ta ce, "Ku koma gida, 'ya'yana mata. Don me za ku tafi tare da ni?
Zan ƙara samun waɗansu 'ya'ya maza da za su zama mazanku ne? 12 Ku koma gida
'ya'yana mata; na tsufa ainun da zan sāke samun wani miji. Ko ma na yi tsammani
har yanzu ina da bege, ko ma na sami miji a wannan dare na kuma haifi 'ya'ya maza,
13 za ku jira sai sun yi girma? Za ku ci gaba da kasance babu aure saboda su? A'a,
'ya'yana mata. Ina da baƙin ciki ƙwarai fiye da ku, domin hannun UBANGIJI ya yi
gāba da ni!"
14 A kan wannan suka sāke ɓarke da kuka. Sa'an nan Orfa ta sumbaci surukarta
ta yi bankwana, amma Rut ta manne mata.
15 Sai Na'omi ta ce, "Duba, 'yar'uwanki ta koma zuwa ga mutanenta da kuma
allolinta. Ki koma tare da ita."
16 Rut Amma Rut ta amsa, "Kada ki roƙe ni in bar ki ko in koma daga gare ki. Inda
za ki, zan tafi, kuma inda za ki zauna, zan zauna. Mutanenki, za su zama mutanena
kuma Allahnki, zai zama Allahna. 17 Inda za ki mutu zan mutu, zan mutu a can
kuma za a binne ni. Bari UBANGIJI ya hukunta ni da tsanani sosai, in wani abu in ba
mutuwa ce ta raba ke da ni ba." 18 Sa'ad da Na'omi ta gane cewa Rut ta ƙudura tǎ
tafi tare da ita, sai ta daina nema tǎ koma.
19 Saboda haka matan biyu suka ci gaba da tafiya sai da suka isa Betlehem. Da suka
isa Betlehem, sai dukan garin ya ruɗe saboda su, matan kuwa suka ce, "Na'omi ce
wannan kuwa?"
20 Ta ce musu, "Kada ku kira ni Na'omi.[†] Ku kira ni Mara[‡] gama Maɗaukaki[§] ya
sa raina ya yi ɗaci sosai. 21 In tafi cikakke, amma UBANGIJI ya dawo da ni ba kome.
Don me kuke kirana Na'omi? UBANGIJI ya wahalshe[*] ni, Maɗaukaki ya kawo mini

[*] **1:1** A gargajiyance alƙalai [†] **1:20** Na'omi yana nufin mai daɗi; haka ma a aya 21. [‡] **1:20** Mara yana nufin ɗaci. [§] **1:20** Da Ibraniyanci an rubuta Shaddai ne a nan. [*] **1:21** Ko kuwa ba da shaida gāba da ni.

masifa.”
22 Na’omi fa ta koma daga Mowab tare da Rut mutuniyar Mowab, surukarta, suka
kai Betlehem a lokacin da ake fara girbin sha’ir.

# 2

*Rut ta sadu da Bowaz*

1 To, fa, Na’omi tana da dangi a gefen mijinta da iyalin Elimelek, mutum mai
martaba, mai suna Bowaz.
2 Sai Rut mutuniyar Mowab ta ce wa Na’omi, “Bari in tafi gonaki in yi kala raguwar
hatsi a bayan duk wanda na sami tagomashi daga gare shi.”
Na’omi ta ce mata, “Ki je, ’yata.” 3 Saboda haka ta tafi ta fara kala a gonaki a bayan
masu girbi. Sai ya zamana, ta sami kanta tana aiki a gonar da take ta Bowaz, wanda
yake daga dangin Elimelek.
4 Sai ga Bowaz ya iso daga Betlehem ya gai da masu girbi, “UBANGIJI yă kasance
tare da ku!”
Sai suka amsa, “UBANGIJI yă albarkace ka!”
5 Sai Bowaz ya tambayi shugaban masu girbinsa, “Wace yarinya ce wannan?”
6 Shugaban ya amsa, “Ita ce mutuniyar Mowab da ta zo daga Mowab tare da Na’omi.
7 Ta ce, ‘Ina roƙo a bar ni in bi bayan masu girbin in yi kala.’ Haka ta shiga cikin
gonar ta kuwa yi aiki tun da safe har zuwa yanzu, sai ɗan hutun da ta yi kaɗan.”
8 Saboda haka Bowaz ya ce wa Rut, “’Yata, ki saurare ni. Kada ki tafi ki yi kala a
wani gona, kada kuma ki tafi daga nan. Ki tsaya nan tare da ’yan matana bayi. 9 Ki
lura da gonar da mutanena suke girbi, ki bi su tare da ’yan matana. Na riga na faɗa
wa mazan kada su taɓa ke. Kuma duk sa’ad da kika ji ƙishirwa, ki tafi ki ɗebo ruwa
daga tulunan da mazan suka cika.”
10 Jin haka, sai ta rusuna da fuskata har ƙasa ta ce, “Me ya sa na sami irin wannan
tagomashi a idanunka da har ka lura da ni, ni da nake baƙuwa?”
11 Bowaz ya amsa, “An faɗa mini duka game da abin kika yi domin surukarki tun
mutuwar mijinki, yadda kika bar mahaifinki da mahaifiyarki da kuma ƙasarki kika
zo ki yi zama da mutanen da ba ki taɓa sani ba. 12 Bari UBANGIJI yă sāka maka saboda
abin da ka yi. Bari UBANGIJI, Allah na Isra’ila yă sāka maka a yalwace, a ƙarƙashin
fikafikan da ka sami mafaka.”
13 Ta ce, “Bari in ci gaba da samun tagomashi a idanunka ranka yă daɗe. Ka
ta’azantar da ni ka kuma yi wa baranyarka magana mai alheri ko da yake ban kai
matsayi ɗaya daga cikin bayinka ’yan mata ba.”
14 A lokacin cin abinci Bowaz ya ce mata, “Zo nan. Ki ɗebo burodi ki tsoma cikin
ruwan inabi.”
Da ta zauna tare da masu girbin, sai ya ba ta gasasshe hatsi. Ta ci duk abin da
take so har ta bar ragowa. 15 Da ta tashi don tă yi kala, sai Bowaz ya yi umarni wa
samarinsa cewa, “Ko ta tara daga cikin dammuna, kada ku wulaƙanta ta. 16 Ku kuma
riƙa zarar mata waɗansu daga dammunan don ta ɗauka, kada ku kwaɓe ta.”
17 Saboda haka Rut ta yi kala a gonar har yamma. Sa’an nan ta sussuka hatsin
sha’ir da ta kalata ta sami kamar efa.* 18 Ta ɗauka ta koma gari sai surukarta ta ga
yawan abin da ta kalato. Rut kuma ta fitar da ragowar abin da ta ci bayan ta ƙoshi
ta ba ta.
19 Surukarta ta tambaye ta, “Ina kika yi kala a yau? Ina kika yi aiki? Albarka ta
tabbata ga mutumin nan ta ya lura da ke!”
Sai Rut ta faɗa wa surukarta game da wurin wanda ta yi ta aiki. Ta ce, “Sunan
mutumin da na yi aiki da shi a yau Bowaz ne.”

---

* **2:17** Wato, kusan bushel uku bisa biyar (Kamar lita 22)

20 Sai Na'omi ta ce wa surukarta, "UBANGIJI yă yi masa albarka! Bai daina nuna
alheri ga masu rai da matattu ba." Ta ƙara da cewa, "Wannan mutum danginmu ne
na kusa; shi ɗaya daga cikin danginmu mai fansa."
21 Sa'an nan Rut mutuniyar Mowab ta ce, "Ya ma ce mini, 'Ki riƙa bin ma'aikatana
sai sun ƙare yin girbin dukan hatsina.' "
22 Na'omi ta ce wa Rut surukarta, "Zai fi miki kyau, 'yata ki riƙa tafiya da 'yan
matansa, domin a gonar wani dabam mai yiwuwa a yi miki lahani."
23 Saboda haka Rut ta tsaya kusa da bayi mata na Bowaz don tă yi kala sai da girbin
sha'ir da na alkama suka ƙare. Ta kuwa zauna tare da surukarta.

# 3

*Rut da Bowaz a masussuka*

1 Wata rana Na'omi surukar Rut ta ce mata, "'Yata, bai kamata in nema miki gida,*
inda za a tanada miki da kyau? 2 Bowaz wanda kike aiki da bayinsa 'yan mata ba
danginmu ne na kusa ba? Da daren yau zai sussuka sha'ir nasa a masussuka. 3 Ki
yi wanka ki fesa turare, ki kuma sa tufafinki mafi kyau. Sa'an nan ki gangara zuwa
masussuka, amma kada ki bari yă san cewa kina a can sai ya gama ci da sha. 4 Sa'ad
da ya kwanta, ki lura da inda yake kwance. Sa'an nan ki tafi ki buɗe ƙafafunsa ki
kwanta. Zai faɗa miki abin da za ki yi."
5 Rut ta amsa ta ce "Zan yi abin da kika faɗa." 6 Saboda haka ta gangara zuwa
masussuka ta kuma yi dukan abin da surukarta ta ce ta yi.
7 Sa'ad da Bowaz ya gama ci da sha yana kuma cikin farin ciki, sai ya tafi ya kwanta
a ƙarshen tarin hatsi. Rut kuwa ta sulalle ta je ta buɗe ƙafafunsa ta kwanta. 8 Da
tsakar dare sai wani abu ya firgitar da mutumin, ya kuwa juya sai ya tarar da mace
kwance a ƙafafunsa.
9 Sai ya yi tambaya ya ce, "Ke wace ce?"
Ta amsa ta ce, "Ni ce baranyarka Rut, ka rufe ni ta mayafinka da yake kai dangi,
mai fansa ne na kusa."
10 Sai ya amsa ya ce, "UBANGIJI yă albarkace ki 'yata. Wannan alheri ya fi wannan
da kika nuna da farko. Ba ki gudu kin bi saurayi, mai arziki ko matalauci ba. 11 Yanzu
kuwa 'yata kada ki ji tsoro. Zan yi miki dukan abin da kika roƙa. Dukan 'yan'uwana
na gari sun san cewa ke mace ce mai halin kirki. 12 Ko da yake gaskiya ne ni dangi
ne na kusa, amma akwai dangi mai fansa mafi kusa fiye da ni. 13 Ki kwana a nan,
da safe kuwa in yana so yă fansa, to, da kyau, sai yă fansa. Amma in ba ya niyya,
tabbatacce, na rantse da UBANGIJI mai rai zan yi. Ki kwanta a nan sai da safe."
14 Saboda haka ta kwanta a ƙafafunsa sai da safe, amma ta tashi kafin a gane wani,
sai ya ce, "Kada ki bar wani yă san cewa mace ta zo masussuka."
15 Ya kuma ce, "Ki kawo gyalenki da kika yafa ki shimfiɗa shi a nan." Sa'ad da ta
yi haka, sai ya zuba mudu shida na sha'ir ya sa mata a kai. Sa'an nan ya† koma gari.
16 Sa'ad da Rut ta koma wurin surukarta Na'omi ta tambaye ta "Yaya aka yi 'yata?"
Sai ta faɗa mata dukan abin da Bowaz ya yi mata 17 ta kuma ƙara da cewa, "Ya
ba ni waɗannan mudu shida na sha'ir, yana cewa, 'Kada ki koma wurin surukarki
hannu wofi.' "
18 Sai Na'omi ta ce, "Ki jira, 'yata, sai kin ga abin da zai faru. Gama mutumin ba
zai huta ba sai an warware batun a yau."

# 4

*Bowaz ya auri Rut*

* **3:1** Da Ibraniyanci an rubuta in sami miki hutu ne a nan. † **3:15** Da yawa cikin rubuce-rubucen hannun Ibraniyanci, yawancin rubuce-rubucen Ibraniyanci, Bulget da na Siriyak suna da ita ce a nan.

1 Ana cikin haka Bowaz ya haura zuwa ƙofar gari ya tafi ya zauna a can. Sa'ad
da dangi mai fansan da ya yi zance ya iso, Bowaz ya ce, "Zo nan abokina ka zauna."
Saboda haka ya ratso ya zauna.
2 Bowaz kuwa ya kira dattawa guda goma na garin ya ce, "Ku zauna a nan," suka
kuwa zauna. 3 Sa'an nan ya ce wa dangin nan mai fansa, "Na'omi, wadda ta dawo
daga Mowab, tana so ta sayar da filin da yake na ɗan'uwanmu Elimelek. 4 Na ga
ya kamata in jawo hankalinka ga batun in kuma ba da shawara ka saye shi a gaban
waɗannan da suke zazzaune a nan da kuma a gaban dattawan jama'a. In kana so
ka fanshe shi, to, sai ka yi. Amma in ba za ka* yi ba, sai ka faɗa mini, don in sani.
Gama babu wani mai izinin yin haka sai kai, ni ne kuwa na biye."

Sai ya ce, "Zan fansa."

5 Sa'an nan Bowaz ya ce, "A ranar da ka saya filin daga Na'omi da kuma daga
Rut mutuniyar Mowab, ka sayi† gwauruwar marigayin nan, domin ka riƙe sunan
marigayin da kuma kayansa."
6 Da jin haka, sai dangin nan mai fansa ya ce, "To, ba zan iya fanshe shi ba don
kada in yi wa nawa mallakar rauni. Za ka iya fanshe shi wa kanka. Ni dai ba zan iya
ba."
7 (To, a kwanakin can a Isra'ila, domin a tabbatar da fansa da kuma musayar da
mallaka, mutum zai cire takalminsa ya ba wa ɗayan. Wannan ita ce hanyar tabbatar
da al'amarin a hukumance a cikin Isra'ila.)
8 Saboda haka dangin nan mai fansa ya ce wa Bowaz, "Saye shi wa kanka." Sai ya
cire takalminsa.
9 Sa'an nan Bowaz ya yi shela wa dattawa da kuma dukan mutane, "A yau ku
ne shaidu cewa na saya daga Na'omi dukan mallakar Elimelek, Kiliyon da kuma
Malon. 10 Na kuma ɗauki Rut mutuniyar Mowab, gwauruwar Malon a matsayin
matata domin sunan mamaci da kuma mallakarsa yă ci gaba, domin kada sunansa
yă ɓace daga cikin iyali ko daga tarihin gari. A yau ku ne shaidu!"
11 Sai dattawan da kuma dukan waɗanda suke a ƙofar suka ce, "Mu shaidu ne.
Bari UBANGIJI yă sa macen da take zuwa cikin gidanka ta zama kamar Rahila da
Liyatu, waɗanda tare suka gina gidan Isra'ila. Bari ka sami martaba a cikin Efrata
ka kuma zama sananne cikin Betlehem. 12 Ta wurin 'ya'yan da UBANGIJI zai ba ka ta
wurin wannan mace, bari iyalinka yă zama kamar na Ferez, wanda Tamar ta haifa
wa Yahuda."

### *Na'omi ta sami yaro*

13 Sai Bowaz ya ɗauki Rut ta kuwa zama matarsa. Sa'an nan ya kwana da ita,
UBANGIJI kuma ya sa ta yi ciki, ta haifi ɗa. 14 Mata suka ce wa Na'omi, "Yabo ya
tabbata ga UBANGIJI, wanda a wannan rana bai bar ki ba tare da dangi mai fansa ba.
Allah yă sa yă zama sananne a dukan Isra'ila! 15 Zai sabunta rayuwarki yă adana ki
a tsufanki. Gama surukarki wadda take ƙaunarki wadda kuma take mafi kyau gare
ki fiye da 'ya'ya maza bakwai, ta haife shi."
16 Sai Na'omi ta ɗauki yaron, ta kwantar da shi a cinyarta ta kuma kula da shi.
17 Matan da suke zama a wurin suka ce, "Na'omi ta sami yaro." Suka kuwa ba shi
suna Obed. Shi ne ya haifi Yesse, mahaifin Dawuda.

18 Ga asalin zuriyar Ferez.

Ferez shi ne mahaifin Hezron,
19 Hezron ya haifi Ram,

---

* **4:4** Da yawa cikin rubuce-rubucen hannun Ibraniyanci, Seftuwajin, Bulget da na Siriyak, yawancin rubuce-rubucen Ibraniyanci, suna da shi ne a nan. † **4:5** Da Ibraniyanci, Bulget da na Siriyak, Na'omi, ka saya Rut mutuniyar Mowab

Ram ya haifi Amminadab,
20 Amminadab ya haifi Nashon,
Nashon ya haifi Salmon,‡
21 Salmon ya haifi Bowaz,
Bowaz ya haifi Obed,
22 Obed ya haifi Yesse,
Yesse kuwa ya haifi Dawuda.

‡ **4:20** Kaɗan daga cikin rubuce-rubucen Ibraniyanci waɗansu rubuce-rubucen Seftuwajin da Bulget (dubi kuma aya 21 da kuma Seftuwajin na 1Tar 2.11); yawancin rubuce-rubucen Ibraniyanci suna da Salma ne.

# 1 Sama’ila

*Haihuwar Sama’ila*

1 Akwai wani mutum daga Ramatayim, mutumin Zuf[*] daga ƙasar tuddan Efraim,
sunansa Elkana, ɗan Yeroham, shi jikan Elihu ɗan Tohu, tattaɓa kunnen Zuf,
mutumin Efraim. 2 Yana da mata biyu, ɗaya sunanta Hannatu, ɗayan kuwa ana
kiranta Feninna. Ita Feninna tana da ’ya’ya, amma Hannatu ba ta da ’ya’ya.
3 Shekara-shekara wannan mutum yakan haura daga garinsa zuwa Shilo domin
yin sujada da miƙa hadayu ga UBANGIJI Maɗaukaki. A can kuwa ’ya’yan Eli maza
biyu, Hofni da Finehas su ne firistoci na UBANGIJI. 4 Duk sa’ad da rana ta kewayo
don Elkana yă miƙa hadaya, yakan ba da kashin nama ga matarsa Feninna da dukan
’ya’yanta maza da mata. 5 Amma Hannatu kuwa sai yă ba ta babban rabo gama
yana ƙaunarta ko da yake UBANGIJI ya kulle mahaifarta. 6 Saboda UBANGIJI ya kulle
mahaifarta, sai kishiyarta ta dinga tsokanarta don tă ba ta haushi. 7 Wannan ya ci
gaba shekara da shekaru. Duk lokacin da Hannatu ta haura zuwa haikalin UBANGIJI,
sai kishiyarta tă tsokane ta har tă yi ta kuka tă kuma ƙi cin abinci. 8 Elkana mijinta
kuwa yakan ce mata, “Hannatu don me kike kuka? Me ya sa ba za ki ci abinci ba?
Don me kika karaya? Ashe, ban fi ’ya’ya goma a gare ki ba?”
9 Wata rana sa’ad da suka gama ci da sha a Shilo, Hannatu ta miƙe tsaye. Eli firist
kuwa yana zaune a kujera a bakin ƙofar haikalin UBANGIJI. 10 A cikin baƙin ciki,
Hannatu ta yi kuka mai zafi ta yi addu’a ga UBANGIJI. 11 Ta yi ta cewa, “Ya UBANGIJI
Maɗaukaki. In har ka dubi baƙin cikin baiwarka, ka tuna da ni, ba ka kuma manta
da baiwarka ba, amma ka ba ta ɗa, ni ma zan miƙa shi ga UBANGIJI dukan rayuwarsa,
aska kuwa ba za tă taɓa kansa ba.”
12 Yayinda take addu’a ga UBANGIJI, Eli ya lura da bakinta. 13 Hannatu tana addu’a a
zuci, ba a jin muryarta, sai leɓunanta ne kawai suna motsi. Eli kuwa ya yi tsammani
ta bugu ne. 14 Sai ya ce mata, “Har yaushe za ki ci gaba da maye? Ki daina shan
ruwan inabi.”
15 Hannatu ta ce, “Ba haka ba ne, ranka yă daɗe, ni mace ce da take cikin matsala
ƙwarai da gaske. Ban sha ruwan inabi ba, ko wani abu mai sa maye, ina dai faɗa
wa UBANGIJI abin da yake damuna ne. 16 Kada ka yi zato baiwarka ’yar iska ce. Ina
addu’a a nan saboda yawan azaba da baƙin cikin da nake ciki.”
17 Eli ya ce, “In haka ne, to, ki sauka lafiya, Allah na Isra’ila kuma yă ba ki abin da
kika roƙa daga gare shi.”
18 Ta ce, bari baiwarka tă sami tagomashi a idonka. Sai ta yi tafiyarta ta je ta ci
wani abu, fuskarta kuwa ba tă ƙara kasance da baƙin ciki ba.
19 Kashegari da sassafe suka tashi suka yi sujada a gaban UBANGIJI, sai suka koma
garinsu a Rama. Elkana kuwa ya kwana da matarsa Hannatu, UBANGIJI kuma ya tuna
da ita. 20 Ana nan sai Hannatu ta yi ciki, ta kuma haifi ɗa. Ta ba shi suna Sama’ila;
tana cewa, “Domin na roƙe shi daga wurin UBANGIJI.”
21 Da shekara ta kewayo, sai Elkana da iyalinsa suka sāke tafi Shilo domin su yi
hadaya ga UBANGIJI, yă kuma cika alkawarin da ya yi. 22 Hannatu kuwa ba tă bi su
ba. Ta gaya wa mijinta cewa, “Sai bayan na yaye yaron, zan kai shi in miƙa shi a
gaban UBANGIJI, yă kuma kasance a wurin koyaushe.”
23 Elkana mijinta ya ce mata, “Ki yi abin da kika ga ya fi miki kyau. Ki jira har sai
bayan kin yaye shi. UBANGIJI dai ya cika maganarsa.” Saboda haka matar ta tsaya a
gida, ta yi ta renon ɗanta har ta yaye shi.

[*] **1:1** Ko kuwa daga Ramatayim Zufim

24 Bayan ta yaye shi, sai ta ɗauki yaron tare da bijimi bana uku, da mudun gari, da
salkan ruwan inabi, ta kawo su a gidan UBANGIJI a Shilo. 25 Bayan an yanka bijimin,
sai suka kawo yaron wurin Eli. 26 Sai ta ce masa, "Ranka yă daɗe, ba ka gane ni ba?
Ai, ni ce matar da ta taɓa tsayawa a gabanka, tana addu'a ga UBANGIJI. 27 Wannan
yaron ne na roƙa daga wurin UBANGIJI, ya kuwa ba ni abin da na roƙa daga gare shi.
28 Saboda haka, na ba da shi ga UBANGIJI muddin ransa, zai zama na UBANGIJI." A can
kuwa ya yi wa UBANGIJI sujada.

# 2

*Addu'ar Hannatu*

1 Sai Hannatu ta yi addu'a ta ce,
"Zuciyata tana farin ciki a cikin UBANGIJI;
a cikin UBANGIJI an sa ina jin daɗi ƙwarai.
Na buɗe bakina na yi wa abokan gābana dariya.
Kai! Ina murna domin ka cece ni!

2 "Babu wani mai tsarki kamar UBANGIJI
babu wani, in ban da kai;
babu wani dutse kamar Allahnmu.

3 "Ka daina maganganu na girman kai
ka kuma daina faɗin kalmomin ɗaga kai;
gama UBANGIJI Allah ne masani
daga gare shi kuma ana auna ayyuka.

4 "An kakkarya bakkuna masu yaƙi,
amma su da ka raunana an ba su makaman ƙarfi.
5 Waɗanda a dā suna da abinci sosai; yanzu suna ƙodago saboda abinci,
masu fama da yunwa kuwa sun daina jin yunwa.
Ita da take bakararriya, ta haifi 'ya'ya bakwai
amma ita da tana da 'ya'ya da yawa, ta zama mai baƙin ciki.

6 "UBANGIJI ne ke kawo mutuwa, yă kuma rayar
yana kai ga kabari, yă kuma tā da.
7 UBANGIJI ne yakan aika da talauci da kuma dukiya;
yakan ƙasƙantar yă kuma ɗaukaka.
8 Yakan tā da matalauci daga ƙura,
yă kuma ɗaga mai bukata daga tarin toka;
yă zaunar da su tare da 'ya'yan sarki;
yă kuma sa su gāji mulki na ɗaukaka.

"Harsashin duniya na UBANGIJI ne;
a bisansu ne ya kafa duniya.
9 Zai kiyaye ƙafafun masu tsarki,
amma mugaye za su lalace cikin duhu.

"Ba bisa ga ƙarfi mutum ba ne mutum ke nasara;
10 waɗanda suke gāba da UBANGIJI za su hallaka.
Zai yi musu tsawa daga sama,
UBANGIJI zai hukunta dukan duniya.

"Zai ba wa sarkinsa ƙarfi,
yă kuma ɗaukaka shafaffensa."
11 Sa'an nan, Elkana ya koma gida a Rama amma yaron ya yi hidima a gaban
UBANGIJI a ƙarƙashin Eli firist.

### *Muguntar 'ya'yan Eli*

12 'Ya'yan Eli firist, mutane ne masu mugunta. Ba su ɗauki UBANGIJI a bakin kome
ba. 13 Al'ada ce ga firistoci da mutane cewa in wani ya miƙa hadaya, yayinda nama
yake kan wuta, bawan firist zai zo da babban cokali mai yatsu, 14 zai soka cokali mai
yatsun a tukunyar, ko butar da ake dafan naman. Duk abin da cokali mai yatsun ya
cako daga tukunyar, ya zama na firist. Haka aka yi ta yi wa Isra'ilawan da suka zo
miƙa hadaya a Shilo. 15 Tun ma kafin a ƙona kitse, bawan firist yakan zo yă ce wa
mutumin da yake miƙa hadaya, "Ka ba wa firist nama domin yă gasa, ba zai karɓi
dafaffen nama daga wurinka ba, sai ɗanye."
16 In kuwa mutumin ya ce masa, "Bari kitse yă ƙone tukuna, sa'an nan ka ɗiba duk
abin da kake so." Sai bawan yă ce masa, "A'a, ka ba ni yanzu, in ka ƙi kuwa zan ɗiba
ƙarfi da yaji."
17 Wannan zunubin samarin ya yi muni ƙwarai a gaban UBANGIJI, domin sun
wulaƙanta hadayar UBANGIJI, ƙwarai da gaske.
18 Amma yaron nan Sama'ila, yana hidima a gaban UBANGIJI yana sanye da efod na
lilin. 19 Kowace shekara mahaifiyarsa takan ɗinka 'yar taguwa ta kai masa sa'ad da
ita da mijinta suka je miƙa hadaya ta shekara. 20 Eli yakan sa wa Elkana da matarsa
albarka, yă ce, UBANGIJI yă ba ka waɗansu 'ya'ya ta wurin matan nan, maimakon
wanda ta roƙa daga UBANGIJI, ta kuma ba da shi ga UBANGIJI. Bayan haka sai su koma
gida. 21 Hannatu kuwa ta sami alfarma daga UBANGIJI. Ta yi ciki. Ana cikin haka
Sama'ila kuwa sai girma yake ta yi a gaban UBANGIJI.
22 To, Eli kuwa ya tsufa ƙwarai, yana kuma jin labari duk abin da 'ya'yansa suke
yi wa dukan Isra'ila, da yadda suke lalata da matan da suke hidima a bakin ƙofar
Tentin Sujada. 23 Saboda haka ya ce musu, "Don me kuke yin waɗannan abubuwa?
Na sami labari daga wurin mutane a kan duk ayyukan muguntanku. 24 A'a, 'ya'yana
ba labari mai kyau nake ji cikin mutanen UBANGIJI ba. 25 In mutum ya yi wa wani
laifi Allah yakan kāre shi; amma in mutum ya yi wa UBANGIJI zunubi wa zai kāre
shi?" Duk da haka, 'ya'yansa ba su kula da gargaɗin mahaifinsu ba, domin nufin
UBANGIJI ne yă hallaka su.
26 Yaron nan Sama'ila ya dinga girma cikin kwarjini da cikin tagomashi a gaba
UBANGIJI da mutane.

### *Annabcin a kan gidan Eli*

27 Wani mutum ya zo wurin Eli ya ce masa, "Ga abin da UBANGIJI ya ce, 'Ashe ban
bayana kaina sosai ga mahaifinka lokacin da yake a Masar a ƙarƙashin Fir'auna ba?
28 Na zaɓi mahaifinka daga cikin dukan kabilar Isra'ila yă zama firist nawa don yă yi
hidima a bagade, don yă ƙona turare mai ƙanshi, don kuma yă sanya doguwar riga
a gabana. Na kuma ba wa iyalin mahaifinka dukan hadaya ta ƙonawa da Isra'ila
suka miƙa. 29 Don me kuke rena hadayata da sadakokina da na ƙayyade domin
mazaunina? Don me kake girmama 'ya'yanka fiye da ni ta wurin cinye sashe mafi
kyau na kowane hadayar da mutanena Isra'ila suka miƙa?'
30 "Saboda haka UBANGIJI Allah na Isra'ila ya ce, 'Na yi alkawari cewa gidanka da
gidan mahaifinka za su yi mini hidima a gabana har abada.' Amma, yanzu Allah
ya ce, ba zai yiwu ba; waɗanda suke girmama ni; Ni ma zan girmama su. Amma
waɗanda suke ƙasƙantar da ni, haka za a ƙasƙantar da su. 31 Lokaci yana zuwa
sa'ad da zan rage ƙarfinka da ƙarfin iyalin gidan mahaifinka. Domin kada a sāke

samun tsohon mutum a zuriyarka. 32 Za ka zama da ɓacin rai a mazaunina ko da
yake za a yi wa Isra'ila alheri. A zuriyarka ba za a taɓa samun tsohon mutum ba.
33 Kowannenku da ban kashe daga hidima a bagadena ba, za a bar shi don yǎ cika
idanunka da hawaye da kuma baƙin ciki, dukan sauran zuriyarka kuwa za su mutu
a ƙuruciyarsu.
34 " 'Abin da kuma ya faru da 'ya'yanka biyu Hofni da Finehas zai zama alama a
gare ka; saboda mutuwarsu za tǎ zama a rana ɗaya. 35 Zan tayar wa kaina amintaccen
firist wanda zai aikata abin da nake so yǎ yi, zan kuwa ba shi zuriya da koyaushe za
su yi aiki a gaban zaɓaɓɓen sarkina. 36 Sa'an nan duk wanda ya rage a zuriyarka
zai zo yǎ durƙusa a gabansa yǎ roƙi kuɗi da abinci, zai kuma roƙa a yardar masa yǎ
taimaki firistoci da aiki domin yǎ sami abin da zai ci.' "

# 3

*Ubangiji ya kira Sama'ila*

1 Yaron nan Sama'ila ya yi hidima a gaban Ubangiji a ƙarƙashin Eli. A waɗannan
kwanaki kuwa jin magana daga wurin Ubangiji ba safai ba, babu kuma wahayi da
yawa.
2 Wata rana da dare Eli da idanunsa sun kusa makancewa har ba ya iya gani sosai
yana kwance a inda ya saba. 3 Fitilar Allah kuwa tana ci, ba tǎ mutu ba tukuna,
Sama'ila kuma na kwance a haikali na Ubangiji inda akwai akwatin Allah. 4 Sai
Ubangiji ya kira Sama'ila.

Sama'ila ya amsa ya ce, "Ga ni." 5 Sai ya ruga wajen Eli ya ce, "Ga ni, gama ka kira
ni."

Eli ya ce, "Dana ban kira ba, je ka kwanta". Saboda haka ya tafi ya kwanta.

6 Ubangiji ya sāke kiransa ya ce, "Sama'ila!" Sama'ila ya tashi kuma ya je wurin
Eli ya ce, "Ga ni, gama ka kira ni."

Amma Eli ya ce, "Ban kira ka ba, ɗana koma ka kwanta."

7 Sama'ila dai bai riga ya san Ubangiji ba tukuna. Ba a kuma taɓa bayyana maganar
Ubangiji a gare shi ba tukuna ba.

8 Ubangiji ya kira Sama'ila sau na uku, Sama'ila kuma ya tashi ya tafi wurin Eli,
"Ga ni, gama ka kira ni."

Sai Eli ya gane cewa Ubangiji ne ke kira yaron. 9 Saboda haka, Eli ya gaya wa
Sama'ila cewa, "Je ka kwanta, in kuma ya kira ka, ka ce masa, 'Ya Ubangiji ka
yi magana gama bawanka yana saurara.' " Sama'ila ya koma ya kwanta a wurin
kwanciyarsa.

10 Ubangiji kuma ya zo ya tsaya a wurin, yana kira ya ce, "Sama'ila, Sama'ila!"
Kamar yadda ya kira a lokutan baya.

Sai Sama'ila ya ce, "Yi magana gama bawanka yana saurara."

11 Ubangiji ya ce wa Sama'ila, "Duba ina dab da yin wani abu a Isra'ila da zai sa
kunne kowa da yake ji, yǎ ji tsoro. 12 A ranar zan cika dukan maganar da na yi game
da Eli da iyalinsa, daga farko har ƙarshe. 13 Gama na gaya masa zan hukunta gidansa
har abada saboda zunubin da yake sane da shi; 'ya'yansa sun wulaƙantar da kansu,
shi kuma bai tsawata musu ba. 14 Saboda haka na rantse a kan gidan Eli, 'Ba za a
taɓa shafe laifin gidan Eli da hadaya ko baiko ba.' "

15 Sama'ila kuwa ya kwanta har safe, sa'an nan ya buɗe ƙofofin gidan Ubangiji. Ya
ji tsoro yǎ gaya wa Eli wahayin, 16 amma Eli ya kira shi ya ce, "Sama'ila, ɗana."

Sama'ila ya ce, "Ga ni."

17 Eli ya ce, mene ne ya ce maka? Kada ka ɓoye mini. Allah ya yi da kai har ma fiye
in ka ɓoye mini kome da ya ce maka. 18 Don haka sai Sama'ila ya gaya masa kome

bai ɓoye masa kome ba. Sa'an nan Eli ya ce, "Shi ne UBANGIJI bari yǎ yi abin da ya
yi kyau a gare shi."
19 UBANGIJI kuwa yana tare da Sama'ila har girmansa bai kuma bar ko ɗaya daga
maganarsa ta kāsa cika ba. 20 Dukan Isra'ila daga Dan har Beyersheba suka shaida
amincin Sama'ila annabi ne na UBANGIJI. 21 UBANGIJI kuwa ya dinga bayyana a Shilo,
a nan ya bayyana kansa ga Sama'ila ta wurin maganarsa.

# 4

1 Duk sa'ad da Sama'ila ya yi magana dukan Isra'ila sukan saurare shi.

### *Filistiyawa sun kama akwatin alkawari*

Isra'ilawa suka fita yaƙi da Filistiyawa. Isra'ilawa suka kafa sansani a Ebenezer*,
Filistiyawa kuma a Afek. 2 Filistiyawa suka tunƙuro mayaƙansu domin su sadu
da Isra'ilawa, yaƙi kuwa ya yi tsanani har Isra'ilawa suka sha kashi a hannun
Filistiyawa. Filistiyawa suka kashe Isra'ilawa kusan mutum dubu huɗu a bakin dāgā.
3 Lokacin da mayaƙan suka komo sansani, dattawan Isra'ilawa suka yi tambaya suka
ce, "Me ya sa UBANGIJI ya sa muka sha ɗibga a hannun Filistiyawa? Bari mu kawo
akwatin alkawarin UBANGIJI daga Shilo. Domin yǎ tafi tare da mu yǎ ba mu nasara
kan abokan gābanmu."
4 Saboda haka mutanen suka aika waɗansu maza zuwa Shilo, suka kuwa tafi suka
kawo akwatin alkawarin UBANGIJI Maɗaukaki wanda yake zaune tsakanin Kerubobi.
'Ya'yan Eli biyun nan Hofni da Finehas suna wurin tare da akwatin alkawarin
UBANGIJI.
5 Da aka shigo da akwatin alkawarin UBANGIJI a cikin sansani, sai Isra'ilawa suka
tā da babbar murya har ƙasa ta jijjiga. 6 Da jin wannan, Filistiyawa suka yi tambaya
suka ce, "Me ke kawo wannan ihu mai ƙarfi haka a sansanin Isra'ilawa?"
Da suka gane cewa akwatin alkawarin UBANGIJI ne ya shiga sansanin, 7 sai
Filistiyawa suka ji tsoro, suka ce, "Wani allah ya shiga cikin sansanin. Mun shiga
uku! Ba a taɓa yin wani abu haka ba. 8 Kaiton mu! Wa zai kuɓutar da mu daga
hannun waɗannan manyan alloli? Su ne allolin da suka buga Masarawa da irin
annoba masu yawa a jeji. 9 Ku yi ƙarfin hali, ku yi mazantaka, ku Filistiyawa, domin
kada ku zama bayin Ibraniyawa kamar yadda suke a gare ku. Ku yi mazantaka, ku
yi yaƙi."
10 Saboda haka Filistiyawa suka yi yaƙi, Isra'ilawa kuwa suka sha ɗibga, kowane
mutum kuwa ya gudu zuwa tentinsa. Kisan kuwa ya yi muni ƙwarai. Isra'ilawa
sun rasa mayaƙa dubu talatin. 11 Aka ƙwace akwatin alkawarin UBANGIJI. Aka kuma
kashe 'ya'yan Eli biyu, Hofni da Finehas.

### *Mutuwar Eli*

12 A wannan rana wani mutumin Benyamin ya ruga da bakin dāgā ya shigo Shilo,
taguwarsa a yage, kansa kuma a rufe da ƙasa. 13 Da ya iso sai ga Eli zaune a kujera
kusa da hanya yana kallo, domin tsoron da yake da shi saboda akwatin alkawarin
Allah. Da mutumin ya shigo a garin ya ba da labarin abin da ya faru sai dukan gari
ya ruɗe da ihu.
14 Eli ya ji ihun ya yi tambaya ya ce, mene ne dalilin wannan ihu?
Mutumin ya rugo wurin Eli, 15 wanda yake da shekaru tasa'in da takwas da
haihuwa, idanunsa kuma ƙarfi ya ƙare, baya iya gani.
16 Mutumin ya gaya wa Eli cewa, "Shigowata ke nan daga bakin dāgā. Na kuɓuce
daga can yau ɗin nan."
Eli ya ce, "Me ya faru da 'ya'yana?"

* **4:1** Ebenezer wato, dutsen taimako

17 Mutumin da ya kawo labarin ya ce, "Isra'ilawa sun gudu a gaban Filistiyawa,
mayaƙan kuma sun sha mummunar ɗibga. 'Ya'yanka Hofni da Finehas su ma sun
mutu. Aka kuma ƙwace akwatin alkawarin Allah."
18 Da ya ambaci akwatin alkawarin Allah, sai Eli ya fāɗi da baya daga kujeransa
kusa da ƙofa, wuyarsa ta karye, ya kuma mutu domin ya tsufa ƙwarai. Ya yi
shugabancin Isra'ila shekaru arba'in.
19 Matar Finehas, ɗansa tana da ciki a lokacin ta kuma kusa haihuwa. Sa'ad da ta ji
labari cewa an ƙwace akwatin alkawarin Allah, ta kuma labarin surukinta da mijinta
sun mutu, sai ta shiga naƙuda, ta kuma haihu. Amma naƙuda ta sha ƙarfinta. 20 Da
tana mutuwa, matan da suke lura da ita suka ce, "Kada ki karaya kin haifi ɗa namiji."
Amma ba tă ba da amsa ko tă kula ba.
21 Ta ba wa yaron suna Ikabod, ma'ana "Ɗaukaka ta rabu da Isra'ila", domin an
ƙwace akwatin alkawarin Allah, domin kuma mutuwar surukinta da na mijinta. 22 Ta
ce, "Ɗaukaka ta rabu da Isra'ila, gama an ƙwace akwatin alkawarin Allah."

# 5

### *Akwatin alkawari a Ashdod da Ekron*

1 Bayan Filistiyawa sun ƙwace akwatin alkawarin Allah, sai suka ɗauke shi daga
Ebenezer suka kai shi Ashdod. 2 Sa'an nan suka ɗauki akwatin alkawarin suka kai
shi cikin haikalin gunkinsu Dagon, suka ajiye kusa da Dagon. 3 Kashegari da safe da
mutanen Ashdod suka farka sai ga Dagon ya fāɗi a gaban akwatin alkawarin UBANGIJI.
Sai suka ɗauki Dagon suka ajiye a wurin zamansa. 4 Amma kashegari kuma da safe
suka farka sai ga Dagon ya fāɗi a ƙasa a gaban akwatin alkawarin UBANGIJI! Kansa
ya fashe, hannuwansa kuma sun kakkarye sun zube a madogarar ƙofa; jikinsa ne
kaɗai ya rage. 5 Saboda haka firistocin Dagon da waɗanda suke sujada a haikalin
Dagon ba sa taka bakin ƙofar Dagon a Ashdod har wa yau.
6 Hannun UBANGIJI kuwa ya yi nauyi a bisa Ashdod da kewayenta. Ya kawo hallaka
ga dukansu, ya kuma buga su da marurai. 7 Da mutanen Ashdod suka ga abin da yake
faruwa, sai suka ce, "Lalle Akwatin Alkawarin Allah na Isra'ila ba zai kasance da mu
ba, domin hannunsa yana da nauyi a kanmu da bisan Dagon allahnmu." 8 Saboda
haka suka kira duka shugabannin Filistiyawa suka tambaye su, suka ce, "Me za mu
da akwatin alkawarin Allahn Isra'ila?"
Sai suka amsa suka ce, "A ɗauki akwatin alkawarin Allah na Isra'ila a kai shi Gat."
Sai suka ɗauki akwatin alkawarin Allah na Isra'ila.
9 Amma bayan sun kai shi can, sai hannun UBANGIJI ya yi gāba da birnin, aka jefa
shi cikin wani mawuyacin hali. Ya buga mutanen birnin da marurai, babba da yaro.
10 Sai suka aika da akwatin alkawarin Allah zuwa Ekron.
Yayinda akwatin alkawarin Allah yana shiga cikin Ekron, mutanen Ekron suka yi
ihu, suka ce, "An kawo mana akwatin alkawarin Allah na Isra'ila domin yă kashe mu
da mutanenmu." 11 Saboda haka suka kira ga dukan shugabannin Filistiyawa suka
ce, "Ku komar da akwatin alkawarin Allah na Isra'ila inda ya fito; in ba haka ba zai
kashe mu da mutanenmu." Gama mutuwa ta cika garin da tsoro. Hannun Allah ya
yi nauyi a kansa. 12 Waɗanda ba su mutu ba kuwa, sun kamu da marurai. Kukan
birnin kuwa ta hau har zuwa sama.

# 6

### *An komar da akwatin alkawari a Isra'ila*

1 Lokacin da akwatin alkawarin UBANGIJI ya kai wata bakwai a ƙasar Filistiyawa.
2 Filistiyawa suka kira firistoci da bokaye suka ce, "Me za mu yi da akwatin alkawarin
UBANGIJI? Ku gaya mana yadda za mu komar da shi inda ya fito."

3 Suka ce, in za ku komar da akwatin alkawarin Allah na Isra'ila kada ku komar da
shi hannu wofi; amma ku tabbata kun aika da hadaya don laifi zuwa wurinsa. Sa'an
nan za ku warke ku kuma san dalilin da ya sa bai cire hannunsa a kanku ba.

4 Filistiyawa suka ce, "Wace irin hadaya don laifi za mu aika masa?"

Suka ce, "Marurai biyar na zinariya da ɓeraye biyar na zinariya bisa ga yawan
sarakunan Filistiyawa. Saboda annoba iri ɗaya ce ta buga ku da shugabanninku.
5 Ku yi siffofin marurai da na ɓeraye da suke hallaka gari, ku ba da girma ga Allah na
Isra'ila. Watakila zai ɗauke hukuncinsa daga gare ku da allolinku da kuma ƙasarku.
6 Me ya sa kun taurare kanku kamar yadda Masarawa da Fir'auna suka yi? Da ya ba
su matsanancin wahala, ba su bar Isra'ilawa suka tafi hanyarsu ba?

7 "Yanzu fa ku shirya sabon keken shanu da shanu biyu masu ba wa 'ya'yansu nono,
waɗanda ba a taɓa sa musu karkiya ba. Ku daure keken shanu wa shanun, amma
ku tsare 'yan maruƙansu a gida. 8 Ku ɗauki wani akwati ku sa siffofin zinariyan
nan a ciki, waɗanda za su zama kyautai na shafen laifi, ku ajiye kusa da Akwati na
UBANGIJI. Bayan haka sai ku sa keken shanun da akwatin a hanya, ku bar shi yă
tafi. 9 Amma ku zuba ido ku ga in ya haura zuwa yankinsa, zuwa Bet-Shemesh, to,
Ubangiji ne ya kawo mana babban masifar a kanmu. Amma in bai bi ta nan ba, za
mu san cewa ba shi ne ya buge mu ba, tsautsayi ne kawai."

10 Suka yi haka. Suka ɗauki shanun tatsa guda biyu suka ɗaura musu keken shanu,
suka tsare 'yan maruƙansu a gida. 11 Suka aza akwatin alkawarin Ubangiji a bisa
keken shanun tare da akwatin siffofin ɓerayen zinariya da siffofin maruran. 12 Sai
shanun suka miƙe zuwa Bet-Shemesh. Suka bi hanya daidai, ba su juya dama ko
hagu ba. Shugabannin Filistiyawa suka bi har zuwa iyakar ƙasar Bet-Shemesh.

13 A lokacin kuwa mutanen Bet-Shemesh suna girbin alkamansu a kwari da suka
ɗaga ido suka hangi akwatin alkawarin Ubangiji, sai suka yi farin ciki ganinsa.
14 Keken shanun ya zo filin Yoshuwa a Bet-Shemesh ya tsaya a gefen wani babban
dutse. Mutanen suka faskare keken shanun suka miƙa shanun hadaya ta ƙonawa ga
Ubangiji. 15 Lawiyawa suka saukar da akwatin alkawarin Ubangiji tare da babban
akwati mai siffofin zinariya na ɓeraye da marurai suka ajiye su a kan ƙaton dutse.
A wannan rana mutanen Bet-Shemesh suka miƙa hadaya ta ƙonawa da waɗansu
hadayu ga Ubangiji. 16 Shugabanni biyar na Filistiyawan nan suka ga duk abin da ya
faru, suka koma zuwa Ekron a ranar.

17 Waɗannan su ne siffofi marurai na zinariya waɗanda Filistiyawa suka aika
domin miƙa hadaya don laifi ga Ubangiji, ɗaya domin Ashdod, ɗaya domin Gaza,
ɗaya domin Ashkelon, ɗaya domin Gat, ɗaya kuma domin Ekron. 18 Filistiyawa kuma
suka aika da siffofin ɓeraye biyar na zinariya. Yawan ɓerayen sun yi daidai da yawan
garuruwan sarakunan nan biyar na Filistiyawa. Garuruwan sun ƙunshi waɗanda
aka gina katangar birni kewaye da su, da kuma ƙauyukansu. Babban dutsen da
suka ajiye akwatin alkawarin Ubangiji, ya zama shaida har wa yau a filin Yoshuwa
a Bet-Shemesh.

19 Amma Allah ya kashe waɗansu mutum saba'in na mutanen Bet-Shemesh domin
sun leƙa cikin akwatin alkawarin Ubangiji. Mutane kuwa suka yi makoki domin
Ubangiji ya hallaka mutane da yawa. 20 Mutanen Bet-Shemesh suka yi tambaya suka
ce, wa zai iya tsaya a gaban Ubangiji Allah Mai Tsarki? Wurin wa akwatin alkawari
zai je daga nan?

21 Sai suka aiki manzanni zuwa Kiriyat Yeyarim suka ce, "Filistiyawa sun komo da
akwatin alkawarin Ubangiji, ku zo ku ɗauka ku kai wajenku."

# 7

[1] Mutanen Kiriyat Yeyarim suka ɗauki akwatin alkawarin UBANGIJI. Suka kai
a gidan Abinadab da ke kan tudu, suka keɓe Eleyazar ɗansa yă lura da akwatin
alkawarin UBANGIJI. [2] Akwatin Alkawarin ya daɗe a Kiriyat Yeyarim ya kai shekara
ashirin cif.

*Sama'ila ya ci Filistiyawa da yaƙi a Mizfa*

Sai dukan mutanen Isra'ila suka yi makoki suka nemi UBANGIJI. [3] Saboda haka
Sama'ila ya yi magana da dukan gidan Isra'ila ya ce, in har da zuciya ɗaya kuke
juyowa ga UBANGIJI sai ku raba kanku da baƙin alloli da gunkin nan Ashtarot, ku ba
da kanku ga UBANGIJI. Ku yi masa bauta shi kaɗai, zai kuɓutar da ku daga hannun
Filistiyawa. [4] Sai Isra'ilawa suka rabu da gumakan Ba'al da Ashtarot suka bauta wa
UBANGIJI kaɗai.

[5] Sama'ila ya ce, "Ku tattara dukan Isra'ila a Mizfa, ni kuwa zan yi addu'a ga
UBANGIJI dominku." [6] Sa'ad da suka taru a Mizfa, suka kawo ruwa suka zuba a gaban
UBANGIJI. A wannan rana suka yi azumi suka tuba, suka ce, "Mun yi wa UBANGIJI
zunubi!" Sama'ila kuwa ya zauna a Mizfa ya yi mulkin Isra'ilawa.

[7] Da Filistiyawa suka ji cewa Isra'ila sun taru a Mizfa, sai shugabanninsu suka zo
don su yaƙe Isra'ila. Da Isra'ilawa suka ji labarin, sai suka tsorata saboda Filistiyawa.
[8] Suka ce wa Sama'ila, "Kada ka fasa kai kukanmu ga UBANGIJI Allahnmu saboda mu,
don yă cece mu daga hannun Filistiyawa." [9] Sama'ila ya kama ɗan rago ya miƙa shi
ɗungum hadaya ta ƙonawa ga UBANGIJI. Ya yi roƙo ga UBANGIJI a madadin Isra'ila,
UBANGIJI kuwa ya amsa addu'arsa.

[10] Lokacin da Sama'ila yana miƙa hadaya ta ƙonawa, Filistiyawa suka matso kusa
don su yi yaƙi da Isra'ila. A ranar UBANGIJI ya sa babban tsawa ya ruɗar da Filistiyawa
har suka gudu a gaban Isra'ilawa. [11] Isra'ilawa suka fito a guje daga Mizfa suka fafari
Filistiyawa suka yi ta karkashe su a hanya har kwarin Bet-Kar.

[12] Sa'an nan Sama'ila ya ɗauki dutse ya kafa tsakanin Mizfa da Shen, ya sa masa
suna, Ebenezer ma'ana, "Har zuwa wannan lokaci UBANGIJI ya taimake mu." [13] Ta
haka Isra'ilawa suka ci Filistiyawa. Daga ranan Filistiyawa ba su ƙara yin nasara a
kan Isra'ila ba. UBANGIJI ya yi gāba da Filistiyawa har ƙarshen zamanin Sama'ila.
[14] Filistiyawa suka mayar wa Isra'ila da garuruwan da suka ƙwato, wato, daga Ekron
zuwa Gat, dukan yankin ƙasarsu da yake ƙarƙashin ikon Filistiyawa. Aka kuma sami
zaman lafiya tsakanin Isra'ilawa da Amoriyawa.

[15] Sama'ila kuwa ya ci gaba da mulkin Isra'ila dukan rayuwarsa. [16] Shekara-shekara
Sama'ila yakan fita rangadi zuwa Betel, da Gilgal da Mizfa inda yakan yi musu shari'a.
[17] Amma yakan komo Rama inda gidansa yake, a nan yakan yi wa Isra'ila shari'a. A
nan ne kuma ya gina wa UBANGIJI bagade.

# 8

[1] Da Sama'ila ya tsufa, sai ya naɗa 'ya'yansa maza su zama alƙalan Isra'ila. [2] Sunan
ɗansa na fari Yowel, na biyu kuwa Abiya. Suka yi alƙalanci a Beyersheba. [3] Amma
'ya'yansa ba su bi hanyar mahaifinsu ba. Suka mai da hankalinsu ga neman kuɗi da
cin hanci, suna kuma danne gaskiya.

[4] Sai dukan shugabannin Isra'ila suka taru suka zo wurin Sama'ila a Rama. [5] Suka
ce masa, "Ka tsufa, 'ya'yanka kuma ba sa bin hanyarka, saboda haka sai ka naɗa
sarkin da zai bi da mu kamar yadda sauran ƙasashe suke da su."

[6] Amma Sama'ila bai ji daɗi sa'ad da suka ce, "Ka ba mu sarki da zai bi da mu." Sai
ya yi addu'a ga UBANGIJI. [7] UBANGIJI kuwa ya ce masa, "Ka saurari dukan maganganun
da mutanen suke gaya maka. Ai, ba kai ba ne suka ƙi, ni ne suka ƙi in zama sarkinsu.
[8] Haka suka yi daga tun daga ranar da na fitar da su daga Masar har zuwa yau, suka

ƙi ni, suka bauta wa waɗansu alloli, haka ma suke yi maka. 9 Yanzu ka saurare su
amma ka yi musu kashedi sosai, ka sa su san abin da sarkin da zai bi da su zai yi."
10 Sama'ila kuwa ya ce wa mutanen da suke roƙo yǎ naɗa musu sarki dukan abin
da Ubangiji ya faɗa. 11 Ya ce musu, "Ga abin da sarkin da zai yi mulkinku zai yi. Zai
kwashe 'ya'yanku yǎ sa su yi aiki da kekunan yaƙi da dawakansa, waɗansu za su riƙa
gudu a gaban keken yaƙinsa. 12 Zai sa waɗansu su zama shugabannin mutum dubu-
dubu da kuma na hamsin-hamsin. Waɗansu za su yi masa noma da girbi. Waɗansu
za su ƙera masa makaman yaƙi da kayayyaki don keken yaƙinsa. 13 Zai sa 'ya'yanku
mata yin aikin turare da dafe-dafe da kuma toye-toye. 14 Zai karɓi gonakinku mafi
kyau da gonakin inabinku da gonakin zaitunku yǎ ba wa ma'aikatansa. 15 Zai kuma
karɓi zakan hatsinku da na inabinku yǎ ba shugabannin fadarsa da sauran masu
hidimarsa. 16 Zai ƙwace bayinku maza da mata, da shanunku, da jakunanku mafi
kyau domin su yi masa aiki. 17 Zai karɓi zakan dabbobinku, ku kanku za ku zama
bayinsa. 18 Sa'ad da ranar ta zo, za ku yi kuka ku nemi a fishe ku daga sarkin da
kuka zaɓa, Ubangiji kuwa ba zai ji ku ba."
19 Amma mutanen suka ƙi jin Sama'ila, sai suka ce, "A'a, mu dai, muna son sarki
yǎ bi da mu." 20 Ta haka za mu zama kamar sauran ƙasashe, mu kasance da sarkin
da zai bi da mu, yǎ tafi tare da mu zuwa yaƙe-yaƙe.
21 Da Sama'ila ya ji duk maganganun da mutanen suka faɗa, sai ya mayar wa
Ubangiji. 22 Ubangiji kuwa ya ce, "Ka saurare su, ka naɗa masu sarki."
Sa'an nan Sama'ila ya ce wa mutanen Isra'ila, "Kowa yǎ koma garinsa."

# 9

*Sama'ila ya shafe Shawulu da mai*

1 An yi wani mutum, attajiri daga kabilar Benyamin, sunansa Kish, ɗan Abiyel,
jikan Zeror na iyalin Bekorat daga dangin Afiya. 2 Yana da ɗa mai suna Shawulu,
wani kyakkyawan saurayi. A cikin mutanen Isra'ila ba wanda ya fi shi kyau, ya
kuma fi kowa tsaye.
3 To, ana nan sai jakunan Kish mahaifin Shawulu suka ɓace. Kish ya ce wa ɗansa,
"Tashi ka tafi tare da wani daga cikin bayi, ku nemo jakunan." 4 Suka bi ta ƙasar
tudu ta Efraim, suka ratsa ta ƙasar Shalisha amma ba su same su ba. Suka bi ta ƙasar
Shalim, a can ma ba su same su ba sai suka bi ta ƙasar Benyamin, a can ma ba su
same su ba.
5 Da suka iso gunduman Zuf, sai Shawulu ya ce wa bawan da yake tare da shi, "Zo
mu koma kada mahaifina yǎ bar damuwa a kan jakuna, yǎ shiga damuwa game da
mu."
6 Amma bawan ya amsa ya ce, "Duba, a wannan gari akwai wani mutumin Allah,
ana ganin girmansa ƙwarai kuma duk abin da ya faɗa yakan zama gaskiya. Mu tafi
can wurinsa wataƙila zai gaya mana hanyar da za mu bi."
7 Shawulu ya ce wa bawan, "Idan muka isa can, me za mu ba wa mutumin? Ga
shi abinci guzurinmu duk ya ƙare, ba mu da wani abin da za mu kai wa mutumin
Allahn nan. Me muke da shi?"
8 Bawan ya sāke ce masa, "Duba ina da kwatar azurfar da zan ba wa mutumin
Allah don yǎ gaya mana wace hanya ce za mu bi." 9 (A dā a Isra'ila, in wani yana so
yǎ nemi nufin Allah, mutumin yakan ce, "Zo mu tafi wajen mai duba." Gama wanda
ake ce da shi annabi a yanzu, a dā ana kiransa mai duba ne.)
10 Shawulu ya ce wa bawansa, "Madalla, zo mu tafi." Sai suka kama hanya suka
nufi birnin da mutumin Allah yake.
11 Sa'ad da suke haura tudun zuwa birnin, sai suka sadu da waɗansu 'yan mata
sun fito za su ɗiban ruwa. Sai suka tambaye su, suka ce, "Mai duba yana nan?"

12 'Yan matan suka ce, "I, yana nan, ai, ga shi ma a gabanku, ku hanzarta.
Shigowarsa ke nan a garin, domin yau mutane za su ba da sadaka a bagade a kan
tudu. 13 Da zarar kun shiga garin, za ku same shi kafin yă tafi cin abinci a wurin yin
sadakar, can kan tudu. Gama jama'a ba za su ci ba, sai ya kai can ya sa albarka a
sadakar, sa'an nan waɗanda aka gayyata su ci. Ku haura da sauri, za ku same."
14 Suka haura zuwa birnin, da shigarsu sai ga Sama'ila ya nufo su a hanyarsa ta
zuwa kan tudu.
15 Kafin zuwa Shawulu, UBANGIJI ya riga ya bayyana wa Sama'ila ya ce, 16 "Gobe war
haka zan aiko maka da wani mutum daga ƙasar Benyamin. Ka keɓe shi shugaban
mutanena Isra'ila. Shi zai cece mutanena daga hannun Filistiyawa. Na ga azabar
mutanena gama kukansu ya hauro wurina."
17 Da Sama'ila ya hangi Shawulu, UBANGIJI ya ce masa, "Ga mutumin da na yi maka
magana, shi ne zai bi da mutanena."
18 Shawulu ya sami Sama'ila a hanyar shiga gari, sai ya tambaye shi ya ce, "Ina
roƙonka ka nuna mini gidan mai duba?"
19 Sama'ila ya ce, "Ni ne mai duban, ka yi gaba zuwa ka tudu, gama yau za ka ci
tare da ni, da safe kuma in sallame ka, in gaya muku duk abin da yake a zuciyarku.
20 Game da jakunan da suka ɓace kwana uku kuwa, kada ka damu, an same su. Ga
wane ne Isra'ila ta sa dukan zuciya, in ba ga kai da kuma dukan iyalin mahaifinka
ba?"
21 Shawulu ya ce, "Ashe, ni ba mutumin Benyamin ba ne daga ƙaramar kabila ta
Isra'ila? Dangina kuma ba shi ba ne mafi kakanni a cikin kabilar Benyamin ba? Yaya
za ka faɗa mini irin wannan magana."
22 Sa'an nan Sama'ila ya shiga da Shawulu da baransa ya zaunar da su a gaban
waɗanda aka gayyata, mutanen sun kai wajen mutum talatin. 23 Sama'ila ya ce wa
mai dahuwa, "Kawo naman da na ba ka, wannan da na ce ka ajiye dabam."
24 Sai mai dahuwan ya ɗauko cinya da abin da yake bisanta ya kawo ya ajiye a
gaban Shawulu. Sama'ila ya ce, "Ga abin da aka ajiye dominka. Ka ci, gama an
keɓe shi dominka saboda wannan hidima daga lokacin da na ce, 'Na gayyaci baƙi.' "
Shawulu kuwa ya ci tare da Sama'ila a ranan nan.
25 Bayan suka gangaro daga tudu zuwa cikin gari, Sai Sama'ila ya yi magana da
Shawulu a ɗakin samansa. 26 Da asuba sai suka tashi, Sama'ila ya kira Shawulu daga
ɗakin sama ya ce, "Ka shirya, zan sallame ka." Da Shawulu ya shirya, sai Sama'ila
da Shawulu suka fita waje tare. 27 Suna dab da ƙarshen gari, sai Sama'ila ya ce wa
Shawulu, "Ka ce wa bawanka yă yi gaba, kai ka ɗan dakata a nan tukuna, domin in
ba ka saƙo daga Allah."

# 10

1 Sai Sama'ila ya ɗauki 'yar kwalabar mai, ya zuba man ɗin wa Shawulu a kansa,
ya yi masa sumba yana cewa, "UBANGIJI ya keɓe ka shugaba bisa gādonsa. 2 Sa'ad
da ka rabu da ni yau, za ka sadu da mutum biyu kusa da kabarin Rahila a Zelza, a
yankin Benyamin. Za su ce maka, 'An sami jakunan da ka fita nema, yanzu haka
mahaifinka ya bar damuwa kan jakunan ya koma damuwa a kanka, yana cewa, yaya
zan gan ɗana?'
3 "Sa'an nan za ka ci gaba daga nan sai ka kai wajen babban itace na Tabor.
Waɗansu mutum uku za su sadu da kai a hanyarsu zuwa wurin yin wa Allah sujada
a Betel. Ɗaya yana ɗauke da 'yan awaki uku, ɗaya yana ɗauke da burodi uku, ɗayan
kuma yana ɗauke da salkar ruwan inabi. 4 Za su gaishe ka, su ba ka burodi biyu, kai
kuwa sai ka karɓa.
5 "Bayan wannan, za ka tafi Gebiya ta Allah, inda sansanin Filistiyawa yake. Kana
shiga garin, za ka sadu da jerin gwanon annabawa suna gangarowa daga tudu, ana

kaɗa garaya, ana bugan ganguna, ana hura sarewa, ana kuma bugan molo, a gabansu,
su kuma za su yi ta annabci. 6 Ruhun UBANGIJI zai sauko a kanka da iko, za ka kuma
yi annabci tare da su. Za a canja ka ka zama dabam. 7 Da zarar waɗannan alamu
sun cika, sai ka aikata duk abin da kana iya yi gama Allah yana tare da kai.
8 "Ka sha gabana zuwa Gilgal. Lalle zan gangara wurinka domin in miƙa hadaya
ta ƙonawa da hadayu na salama. Sai ka jira ni kwana bakwai sai na zo wurinka na
kuma gaya maka abin da za ka yi."

### *A naɗa Shawulu ya zama sarki*

9 Da Shawulu ya juya zai bar Sama'ila, sai Allah ya canja wa Shawulu zuciya,
alamun nan kuwa suka cika a ranar. 10 Da suka iso Gibeya, jerin gwanon annabawa
suka sadu da shi Ruhun Allah kuma ya sauko a kansa da iko, sai ya shiga yin annabci
tare da su. 11 Sa'ad da dukan waɗanda suka san shi a dā suka gan shi yana annabci
tare da annabawa, sai suka tambayi juna, suka ce, "Me ya faru da ɗan Kish? Shawulu
ma yana cikin annabawa ne?"
12 Wani mutumin da yake zama a can ya ce, "Wane ne kuma mahaifinsu?" Ta
haka sai wannan ya zama karin magana cewa, "Shawulu ma yana cikin annabawa?"
13 Bayan da Shawulu ya gama annabci sai ya haura ya tafi tudu.
14 Sai ɗan'uwan mahaifin Shawulu ya tambaye shi da baransa ya ce, "Ina kuka je?"
Shawulu ya ce, "Mun tafi neman jakuna, amma da ba mu same su ba sai muka tafi
wurin Sama'ila."
15 Ɗan'uwan mahaifin Shawulu ya ce, "Faɗa mini abin da Sama'ila ya ce maka."
16 Shawulu ya ce, "Ya tabbatar mana cewa an riga an sami jakuna." Amma bai
gaya wa ɗan'uwan mahaifinsa abin da Sama'ila ya ce game da sarauta ba.
17 Sama'ila ta tattara mutanen Isra'ila a gaban UBANGIJI a Mizfa 18 ya ce musu, "Ga
abin da UBANGIJI, Allah na Isra'ila ya ce, 'Na fito da Isra'ila daga Masar, na kuma
cece ku daga hannun Masarawa da dukan mulkokin da suka wahalshe ku.' 19 Amma
yanzu kun ƙi Allahnku wanda ya cece ku daga dukan masifu da wahaloli. Kuka ce,
'Sam, a naɗa mana sarki.' Saboda haka yanzu sai ku zo gaban UBANGIJI kabila-kabila
da iyali-iyali."
20 Sa'ad da Sama'ila ya kawo dukan Isra'ila gaba, kabila-kabila, sai aka zaɓi kabilar
Benyamin ta wurin jefa ƙuri'a. 21 Sai ya kawo kabilar Benyamin gaba, iyali-iyali, aka
zaɓi iyalin Matri. A ƙarshe aka zaɓi Shawulu ɗan Kish. Amma da aka neme shi sai
ba a same shi ba. 22 Suka ƙara nemi bayani daga UBANGIJI suka ce, "Mutumin ya zo
nan kuwa?"
UBANGIJI ya ce, "I, ga shi can, ya ɓuya cikin kayayyaki."
23 Suka ruga suka kawo shi. Da ya tsaya cikin mutane, sai ya fi kowa tsayi.
24 Sama'ila ya ce wa dukan mutane, "Kun ga wanda UBANGIJI ya zaɓa ko? Ba wani
kamar sa a cikin dukan mutane."
Sai mutane suka tā da murya suka ce, "Ran sarki yǎ daɗe."
25 Sama'ila kuwa ya bayyana wa mutane ƙa'idodin sarauta. Ya rubuta su cikin littafi
ya ajiye a gaban UBANGIJI. Sa'an nan ya sallame mutane, kowa ya koma gidansa.
26 Shawulu ma ya tafi gidansa a Gibeya tare da waɗansu jarumawan da Allah ya
taɓa zuciyarsu. 27 Amma waɗansu 'yan iska suka ce, "Yaya wannan mutum zai iya
cetonmu?" Suka rena shi suka ƙi su kawo masa kyautai. Amma Shawulu bai ce uffam
ba.

## 11

### *Shawulu ya ceci birnin Yabesh*

1 Nahash mutumin Ammon ya haura ya kewaye Yabesh Gileyad da yaƙi. Dukan
mutanen Yabesh suka ce masa, "Ka ƙulla amana da mu, mu kuwa za mu bauta maka."

2 Amma Nahash ya ce, "Zan ƙulla amana da ku kawai a kan sharaɗin cewa zan
ƙwaƙulo idon dama na kowannenku, ta haka za a kunyata Isra'ila."
3 Dattawan Yabesh suka ce masa, "Ka ba mu kwana bakwai don mu aika manzanni
a dukan ƙasar Isra'ila idan ba mu sami wanda zai cece mu ba, za mu ba da kanmu
gare ka."
4 Da manzannin suka zo Gibeya garin Shawulu, suka gaya wa mutane wannan
sharaɗin, suka yi kuka mai zafi. 5 A daidai wannan lokacin kuwa Shawulu yana
dawowa daga gona tare da shanunsa na noma, sai ya ce, "Me ya faru, mutane suna
kuka haka?" Sai suka faɗa masa abin da mutanen Yabesh suka faɗa musu.
6 Da Shawulu ya ji, sa Ruhun Allah ya sauko a kansa da iko, ya husata ƙwarai. 7 Ya
ɗauki shanu biyu, ya yayyanka su gunduwa-gunduwa, ya aika da su ko'ina a ƙasar
Isra'ila ta wurin manzanni cewa, "Duk wanda bai fita ya bi Shawulu da Sama'ila
ba, haka za a yi da shanunsa." Mutanen suka ji tsoron UBANGIJI suka fita gaba ɗaya
kamar mutum guda. 8 Mutanen Isra'ila sun kai dubu ɗari uku. Mutanen Yahuda
kuma dubu talatin, sa'ad da Shawulu ya tara su a Bezek.
9 Suka ce wa 'yan aikan da suka zo, "Ku faɗa wa mutanen Yabesh Gileyad, 'Gobe,
kafin rana tă yi zafi, za ku sami ceto.' " Sa'ad da 'yan aikan suka tafi, suka ba da
saƙon nan ga mutanen Yabesh, sai suka farin ciki. 10 Suka ce wa Ammonawa, "Gobe
za mu miƙa wuya gare ku, ku kuma yi duk abin da kuka ga dama."
11 Gari yana wayewa, sai Shawulu ya raba mutane kashi uku, a sa'a ta ƙarshe na
daren sai suka fāɗa wa sansanin Ammonawa, suka kuma karkashe su har lokacin
da rana ta yi zafi. Waɗanda suka kuɓuce kuwa suka warwatsu, har babu biyunsu da
aka bari tare.

*An tabbatar da Shawulu sarki*

12 Sai mutane suka ce wa Sama'ila, "Su wa suka ce, 'Shawulu zai yi mulkinmu?' A
kawo mana su mu kashe."
13 Shawulu ya ce, "Ba wanda zai mutu yau, gama UBANGIJI ya kuɓutar da Isra'ila a
wannan rana."
14 Sai Sama'ila ya ce wa mutane, "Ku zo mu tafi Gilgal, a can za a yi wankan
sarauta." 15 Don haka dukan mutane suka tafi Gilgal, suka tabbatar da Shawulu sarki
a gaban UBANGIJI. A can suka miƙa hadaya ta salama a gaban UBANGIJI, Shawulu
kuwa da dukan Isra'ila suka yi babban liyafa.

# 12

*Jawabin bankwanan Sama'ila*

1 Sama'ila ya ce wa Isra'ilawa duka, "Na saurari abubuwan da kuka faɗa mini, na
kuma naɗa muku sarki. 2 Yanzu kuna da sarki a matsayin shugaba, ni kuwa na tsufa
har da furfura, yarana maza kuma suna tare da ku. Na yi shugabancinku tun ina
yaro. 3 Ga ni a gabanku. Idan na yi wani abin da ba daidai ba sai ku faɗa a gaban
UBANGIJI, da gaban sarkin da ya keɓe. Ko na taɓa ƙwace saniya ko jakin wani? Ko na
taɓa cuce wani, ko in danne hakkinsa? Ko na taɓa cin hanci daga hannun ɗayanku?
Idan na taɓa yi ɗaya daga cikin waɗannan, sai ku faɗa mini, zan kuwa mayar masa."
4 Suka ce, "Ba ka cuci ko danne hakkin kowa ba, ba ka ƙwace kome daga hannun
kowa ba."
5 Sama'ila ya ce musu, "UBANGIJI yă zama shaida a kanku, shafaffensa kuma yă
zama shaida a wannan rana cewa ba ku same ni da wani laifin kome ba."
Suka ce, "I, shi ne shaida."
6 Sa'an nan Sama'ila ya ce wa mutane, UBANGIJI ne ya naɗa Musa da Haruna suka
fitar da kakanninku daga Masar. 7 Yanzu ku tsaya nan zan yi fito-na-fito da ku da
shaida a gaban UBANGIJI kan dukan ayyuka masu alherin da UBANGIJI ya aikata saboda
ku da kakanninku.

8 Bayan da Yaƙub da ’ya’yansa suka shiga Masar suka yi kukan neman taimako
daga Ubangiji, Ubangiji kuwa ya aika musu da Musa da Haruna. Su ne suka kawo
kakanni-kakanninku daga Masar suka zauna a nan.
9 Amma suka manta da Ubangiji Allahnsu, shi kuma ya bashe su a hannun Sisera
shugaban rundunar Hazor da kuma hannun Filistiyawa da sarkin Mowab wanda
suka yi yaƙi da su. 10 Suka yi kuka a gaban Ubangiji suka ce, “Mun yi zunubi mun bar
Ubangiji, muka bauta wa Ba’al da Ashtarot. Amma ka cece mu yanzu daga hannun
abokan gābanmu, mu kuwa za mu bauta maka.” 11 Sai Ubangiji ya aiki Yerub-Ba’al
da Bedan da Yefta da Sama’ila, ya cece ku daga hannun abokan gābanku a kowane
gefe domin ku sami cikakken zaman lafiya.
12 Amma da kuka ga Nahash sarkin Ammonawa yana matsowa yă yaƙe, sai kuka
ce mini, “Sam, muna so sarki yă shugabance mu.” Ko da yake Ubangiji Allahnku ne
yake mulkinku. 13 Yanzu ga sarkinku da kuka zaɓa wanda kuka nema, ga shi Ubangiji
ya naɗa muku sarki. 14 In kuka ji tsoron Ubangiji, kuka bauta masa, kuka yi masa
biyayya, ba ku kuwa ƙi bin umarninsa ba, in kuma ku da sarkin da yake mulkinku
kun bi Ubangiji Allahnku, to, za ku zauna lafiya. 15 Amma in ba ku yi biyayya ga
Ubangiji ba, in kuma kuka ƙi bin umarnansa, fushinsa zai zauna a kanku.
16 Yanzu ku tsaya tsit ku ga abin da Ubangiji ke dab da yi a gabanku. 17 Ba lokacin
yankan alkama ke nan ba? Zan roƙi Ubangiji yă aiko da tsawa da ruwan sama, za
ku kuwa gane wace irin mugunta kuka yi a gaban Ubangiji sa’ad da kuka roƙa a ba
ku sarki.
18 Sai Sama’ila ya roƙi Ubangiji, a ranar kuwa Ubangiji ya aiko da tsawa da ruwan
sama. Dukan mutane suka ji tsoron Ubangiji da kuma Sama’ila.
19 Dukan mutane suka ce wa Sama’ila, “Ka yi addu’a ga Ubangiji Allahnka saboda
bayinka, domin kada mu mutu, gama mun ƙara wa kanmu zunubi da muka roƙa a
yi mana sarki.”
20 Sama’ila ya ce, “Kada ku ji tsoro.” Kun yi waɗannan mugunta duk da haka kada
ku bar bin Ubangiji, amma ku bauta wa Ubangiji da dukan zuciyarku. 21 Kada ku bi
alloli marasa amfani. Ba za su iya yi muku kome nagari ba, ba kuwa za su iya cece
ku ba, gama ba su da amfani. 22 Saboda suna mai girma da Ubangiji yake da shi, ba
zai taɓa ƙin mutanensa ba. Gama Ubangiji ya ji daɗi da ya yi ku mutanensa. 23 Ni
kam ba zai taɓa yiwu in yi wa Ubangiji zunubi ta wurin ƙin yin addu’a dominku ba.
Zan koya muku hanyar da tana da kyau da ta kuma cancanta. 24 Amma ku amince za
ku ji tsoron Ubangiji, ku bauta masa da aniya da dukan zuciyarku, kuna da manyan
abubuwan da ya yi muku. 25 Amma in kuka duƙufa cikin aikin mugunta da ku da
sarkinku za a hallaka ku.

# 13

*Sama’ila ya kwaɓi Shawulu*

1 Shawulu yana da shekara talatin sa’ad da ya zama sarki, ya kuma yi sarautar
Isra’ila shekara arba’in da biyu.
2 Sai ya zaɓi sojoji dubu uku daga jama’ar Isra’ila. Ya keɓe dubu biyu su kasance
tare da shi a Mikmash da kuma a tuddan yankin Betel. Ya kuma bar dubu ɗaya
tare da ɗansa Yonatan a Gibeya a yankin zuriyar Benyamin. Sauran sojojin kuwa
Shawulu ya sallame su su koma gidajensu.
3 Yonatan ya kai wa Filistiyawa hari a Geba, sai Filistiyawa suka sami labarin. Sai
Shawulu ya sa aka busa ƙaho ko’ina a ƙasar ya ce, “Bari Ibraniyawa su ji!” 4 Haka
kuwa dukan Isra’ila suka ji labari cewa, “Shawulu ya kai hari a ƙasar Filistiyawa,
yanzu Isra’ila ta zama abin ƙi ga Filistiyawa.” Aka kira mutane su haɗu da Shawulu
a Gilgal.

5 Sai Filistiyawa suka taru don su yi yaƙi da Isra'ilawa. Suka fito da kekunan-
dawakan yaƙi dubu talatin, da masu hawan dawakai dubu shida, da sojoji masu
yawa kamar yashi a bakin teku. Suka tafi Mikmash a gabashin Bet-Awen, suka kafa
sansani a can. 6 Sa'ad da Filistiyawa suka fāɗa wa Isra'ilawa da yaƙi mai tsanani,
suka sa su cikin wani hali mai wuya, sai Isra'ilawa suka ɓuya a kogwanni, da ciyayi,
da duwatsu, da ramummuka, da rijiyoyi. 7 Waɗansunsu ma suka haye Urdun zuwa
ƙasar Gad da Gileyad.

Shawulu ya zauna Gilgal, dukan ƙungiyoyi sojojin da suke tare da shi suka yi rawan
jiki don tsoro. 8 Ya jira har kwana bakwai bisa ga lokacin da Sama'ila ya bayar. Amma
Sama'ila bai zo Gilgal ba, mutanen Shawulu suka fara watsewa. 9 Sai ya ce, "Ku
kawo mini hadaya ta ƙonawa da hadaya ta salama." Sai Shawulu ya miƙa hadaya
ta ƙonawa. 10 Daidai yana gama miƙa hadaya ke nan sai Sama'ila ya iso. Shawulu
kuma ya fito domin yǎ yi masa maraba.

11 Sama'ila ya ce, "Me ke nan ka yi?"

Shawulu ya ce, "Sa'ad da na ga mutane suna watsewa, kai kuwa ba ka zo cikin
lokaci ba, ga Filistiyawa kuma suna taruwa a Mikmash, 12 sai na yi tunani cewa,
'Yanzu Filistiyawa za su gangaro su fāɗa mini a Gilgal, ga ni kuma ban riga na nemi
nufin UBANGIJI ba.' Shi ya sa ya zama mini tilas in miƙa hadaya ta ƙonawa."

13 Sama'ila ya ce, "Ka yi wauta da ba ka bi umarnin da UBANGIJI Allahnka ya ba
ka ba. Da ka yi haka da UBANGIJI ya tabbatar maka da sarautar Isra'ila har abada.
14 Amma yanzu, masarautarka ba za tǎ dawwama ba, UBANGIJI ya riga ya sami wani
wanda zuciyarsa ke ƙauna, ya naɗa shi shugaban mutanensa gama ba ka bi umarnin
UBANGIJI ba."

15 Sama'ila ya tashi daga Gilgal ya tafi Gibeya a ƙasar Benyamin. Shawulu kuma
ya ƙidaya mutanen da suke tare da shi, yawansu ya kai wajen mutum ɗari shida.

### *Isra'ila ba ta da makamai*

16 Shawulu da ɗansa Yonatan da mutanen da suke tare da shi suka zauna a
Geba ta Benyamin. Sa'an nan Filistiyawa suka yi sansani a Mikmash. 17 Rundunar
mayaƙa uku suka fito daga sansani Filistiyawa. Ɗaya ta nufi Ofra, zuwa ƙasar
Shuwal. 18 Runduna guda kuma ta nufi Bet-Horon, ɗayan kuwa ta nufi iyakar da
take fuskantar Kwarin Ziboyim wajen jeji.

19 Ba a sami maƙeri ɗaya a dukan ƙasar Isra'ila ba domin Filistiyawa sun ce, "In
ba haka ba Ibraniyawa za su ƙera wa kansu takuba ko māsu." 20 Saboda haka dukan
Isra'ila sukan gangara zuwa wajen Filistiyawa domin su gyara bakin garemaninsu,
da fartanansu, da gaturansu, da kuma laujunansu. 21 Duk lokacin da za su gyara
bakin garmansu da fartanyarsu sai sun biya tsabar azurfa* biyu. Haka ma idan za
su gyara gatari ko bakunan abin korar shanun noma sai sun biya tsabar azurfa ɗaya.

22 A ranar da yaƙi ya tashi, ba a sami wanda yake da takobi ko māshi ba a cikin
mutanen da suke tare da Shawulu da Yonatan. Sai dai Shawulu da ɗansa Yonatan
kaɗai.

### *Yonatan ya kai wa Filistiyawa hari*

23 Ana nan sai sojojin Filistiyawa suka fita zuwa mashigin Mikmash.

## 14

1 Wata rana Yonatan ɗan Shawulu ya ce wa saurayin da yake ɗaukar masa
makamai, "Zo mu tafi wajen sansanin Filistiyawa a wancan hayi." Amma bai gaya
wa mahaifinsa ba.

* **13:21** tsabar azurfa. Da Ibraniyanci an rubuta biyu bisa uku na Shekel ne a nan. A zamaninsu wannan kuɗi ne mai yawa.

2 Shawulu kuwa na zaune a gindin itacen rumman a bayan garin Gibeya a Migron.
Tare da shi akwai mutum wajen ɗari shida. 3 A cikinsu akwai Ahiya sanye da efod.
Shi yaron Ikabod ɗan'uwan Ahitub ne, ɗan Finehas, ɗan Eli, firist na UBANGIJI a Shilo.
Ba wanda ya san cewa Yonatan ya tafi wani wuri.
4 A kowane gefe na mashigin da Yonatan ya so yǎ bi zuwa wurin Filistiyawa, akwai
hawa mai tsawo, ana kira ɗaya Bozez, ɗayan kuma ana kira Senet. 5 Hawan da yake
arewa yana fuskantar Mikmash, wanda yake kudu kuma yana fuskantar Geba.
6 Yonatan ya ce wa saurayin mai ɗaukan makamai, "Zo mu haye zuwa mashigin
mutane marasa kaciyan nan, wataƙila UBANGIJI zai yi aiki a madadinmu. Ba abin da
zai iya hana UBANGIJI yin aikin ceto ta wurin mutane masu yawa, ko ta wurin mutane
kaɗan."
7 Mai ɗaukan makaman ya ce, "Ka yi duk abin da yake zuciyarka. Ci gaba, ina tare
da kai gaba da baya."
8 Yonatan ya ce, "To, zo mu haye zuwa wajen mutanen, mu sa su gan mu. 9 In suka
ce mana, 'Ku tsaya nan har mu zo wurinku,' za mu dakata inda muke, ba za mu
haura wajensu ba. 10 Amma in suka ce mana, 'Ku haura wurinmu,' to, sai mu haura,
wannan zai zama mana alama cewa UBANGIJI ya bashe su a hannunmu."
11 Sai suka nuna kansu a sansanin Filistiyawa. Sai Filistiyawa suka ce, "Ku duba
ga Ibraniyawa suna fitowa daga cikin ramummuka inda suka ɓuya." 12 Mutanen da
suke sansanin suka kira Yonatan da mai ɗaukan makamansa da babbar murya suka
ce, "Ku hauro wajenmu, mu kuwa za mu koya muku hankali."
Sai Yonatan ya ce wa mai ɗaukan makamansa, "Biyo ni, gama UBANGIJI ya bashe
su a hannun Isra'ila."
13 Sai Yonatan ya hau dutsen da rarrafe, mai ɗaukan makamansa kuwa yana biye.
Yonatan ya yi ta fyaɗa Filistiyawa da ƙasa, mai ɗaukan makamansa kuma ya yi ta
karkashe su. 14 A wannan karo na farko Yonatan da mai ɗaukan makamansa suka
kashe mutum wajen ashirin a wani fili mai fāɗi rabin kadada.

### *Isra'ila ta watsar da Filistiyawa*

15 Sai tsoro ya kama dukan sojojin Filistiyawa, waɗanda suke cikin sansanin da
waɗanda suke fili, har da waɗanda suke waje, da kuma waɗanda suke kai hari, ƙasa
ta girgiza. Allah ne ya kawo wannan rikicewa.
16 Masu gadin Shawulu a Gebiya da take a Benyamin suka duba sai ga rundunar
Filistiyawa a warwatsewa ko'ina. 17 Sai Shawulu ya ce wa mutanen da suke tare da
shi, "Ku ƙidaya mayaƙa ku ga wane ne ba ya nan." Da suka ƙirga sai suka tarar
Yonatan da mai ɗaukan makamansa ba sa nan.
18 Shawulu ya ce wa Ahiya, "Kawo akwatin alkawarin Allah." (A lokacin akwatin
alkawarin yana tare da Isra'ilawa.) 19 Yayinda Shawulu yake magana da firist kuwa,
harguwa ya yi ta ƙaruwa a sansanin Filistiyawa. Sai Shawulu ya ce wa firist, "Janye
hannunka."
20 Sa'an nan Shawulu da dukan mutanensa suka taru suka tafi yaƙi. Suka tarar
Filistiyawa sun ruɗe suna yaƙi da juna da takubansu. 21 Ibraniyawan da suke tare da
Filistiyawa a dā, waɗanda suka bi Filistiyawan zuwa sansanin yaƙinsu, suka juya,
suka goyi bayan Shawulu da Yonatan sa'ad da yaƙin ya taso. 22 Sa'ad da dukan
Isra'ilawan da suka ɓuya a duwatsu a ƙasar Efraim suka ji labari cewa Filistiyawa
suna gudu, sai suka fito suka fafare su. 23 Haka UBANGIJI ya kuɓutar da Isra'ila a
wannan rana. Yaƙin kuwa ya ci gaba har gaba da Bet-Awen.

### *Yonatan ya sha zuma*

24 A wannan rana, Isra'ilawa suka sha wahala ƙwarai domin Shawulu ya sa mutane
suka yi rantsuwa cewa, "La'ananne ne mutumin da ya ci abinci kafin fāɗuwar rana,

kafin in ɗauki fansa a kan abokan gābana." Don haka ba mutumin da ya ɗanɗana abinci.
25 Dukan rundunar ta shiga kurmi, sai ga zuma a ƙasa. 26 Da suka shiga ciki kurmin,
suka ga zuma tana zubowa, duk da haka ba wanda ya sa yatsansa ya lasa saboda
tsoron rantsuwar da suka yi. 27 Yonatan bai san cewa mahaifinsa ya sa mutane suka
yi rantsuwa ba. Sai ya sa gindin sandan da yake hannunsa a saƙar zuma, ya kai
bakinsa. Nan da nan sai ya ji ƙarfin jiki ya zo masa. 28 Sai wani soja ya gaya masa
cewa, "Mahaifinka ya sa kowa ya yi rantsuwa cewa, 'La'ananne ne mutumin da ya
ci abinci kafin fāɗuwar rana!' Shi ya sa duk sojojin ba su da ƙarfi."
29 Yonatan ya ce, "Mahaifina ya jefa ƙasar cikin matsala. Duba yadda na ji ƙarfin
jiki sa'ad da na ɗanɗana wannan 'yar zuma mana. 30 Da yaya zai kasance ke nan
da a ce an bar sojoji suka ci abincin da suka ƙwace daga abokan gābansu? Ai, da
gawawwakin Filistiyawan da aka kashe sun fi haka."
31 A ranan nan Isra'ilawa suka yi ta kashe Filistiyawa daga Mikmash har zuwa
Aiyalon. Bayan haka gajiya ta kama su sosai saboda yunwa. 32 Sai suka yi warwason
ganima, suka kwashe tumaki, da shanu, da maruƙa, suka yayyanka su, suka ci naman
ɗanye. 33 Sai wani mutum ya ce wa Shawulu, "Duba, ga mutane suna zunubi ga
UBANGIJI, suna cin nama da jini."

Shawulu ya ce, "Kun ci amana. Ku mirgino babban dutse zuwa wurina nan da
nan." 34 Sa'an nan ya ce, "Ku tafi ku faɗa wa jama'a duka, su kawo shanu da tumaki
a nan, su yayyanka, su ci a nan, don kada su yi wa UBANGIJI zunubi da cin nama
ɗanye."

Haka nan kowa ya kawo saniyarsa a daren, ya yanka a can. 35 Sa'an nan Shawulu
ya gina wa UBANGIJI bagade. Wannan ne bagade na farkon da ya gina.
36 Shawulu ya ce, "Mu bi gangara mu fafare Filistiyawa da dare mu washe su har
gari yă waye, mu kuma karkashe kowannensu, kada mu bar wani da rai."

Suka ce, "Ka yi duk abin da ka ga ya fi maka kyau."

Amma firist ya ce, "Bari mu nemi nufin Allah tukuna."
37 Saboda haka Shawulu ya tambayi Allah ya ce, "Mu bi bayan Filistiyawa? Za ka
bashe su a hannun Isra'ila?" Amma Allah bai ba shi amsa a ranar ba.
38 Saboda haka Shawulu ya ce, "Ku zo nan dukanku shugabannin rundunoni, mu
bincika mu san zunubin da ya kawo rashin amsan nan yau. 39 Muddin UBANGIJI
wanda ya ceci Isra'ila yana raye, ko da ɗana Yonatan ne ya yi zunubin, dole yă
mutu." Amma ba ko ɗaya daga cikinsu da ya ce uffam.
40 Sai Shawulu ya ce wa dukan Isra'ilawa, "Ku tsaya a can, ni kuma da Yonatan
ɗana mu tsaya a nan."

Mutanen suka ce, "Ka yi abin da ya fi maka kyau."
41 Sa'an nan Shawulu ya yi addu'a ga UBANGIJI, Allah na Isra'ila ya ce, "Me ya sa
ba ka amsa mini addu'ata a yau ba? Idan wannan laifina ne, ko kuwa na ɗana,
Yonatan, ka nuna mana ta wurin Urim, amma idan laifin mutanen ne ka amsa ta
wurin Tummim." Ba a sami mutane da laifi ba, amma ƙuri'a ta fāɗa a kan Yonatan
da Shawulu. 42 Shawulu ya ce, "Ku jefa ƙuri'a tsakanina da ɗana Yonatan." Sai
ƙuri'ar ta fāɗa a kan Yonatan.
43 Sai Shawulu ya ce wa Yonatan, "Gaya mini mene ne ka yi."

Yonatan ya ce masa, "Na ɗanɗana zuma kaɗan daga gindin sandanta. Yanzu kuwa dole in mutu!"
44 Shawulu ya ce, "Bari hukunci mai tsanani na Allah yă kasance a kaina, in ba ka mutu ba, Yonatan."
45 Amma mutane suka ce wa Shawulu, "A ce Yonatan yă mutu bayan shi ya kawo
babban nasara a Isra'ila? Faufau, muddin UBANGIJI yana raye, ko gashin kansa ɗaya

ba zai fāɗi a ƙasa ba, gama abin da ya yi yau, Allah ne yana tare da shi." Ta haka
mutane suka ceci Yonatan daga mutuwa.
46 Sai Shawulu ya daina bin Filistiyawa, suka koma ƙasarsu.
47 Bayan Shawulu ya hau karagar mulkin Isra'ila, ya yi yaƙi da abokan gābansu
ta kowane gefe. Mowabawa, Ammonawa, mutanen Edom, sarakunan Zoba, da kuma
Filistiyawa. Duk wurin da ya juya, ya hore su. 48 Ya yi jaruntaka sosai, ya ci
Amalekawa da yaƙi, ya kuma ceci Isra'ila daga hannuwan waɗanda suka ƙwace
musu kaya.

### *Iyalin Shawulu*

49 'Ya'yan Shawulu maza su ne, Yonatan, Ishbi, da Malki-Shuwa. Sunan babban
'yarsa ita ce Merab, ƙaramar kuma Mikal. 50 Sunan matarsa kuwa Ahinowam, 'yar
Ahimawaz. Sunan shugaban ƙungiyar sojan Shawulu kuwa Abner ne ɗan Ner, shi
Ner kuwa ɗan'uwan mahaifin Shawulu ne. 51 Mahaifin Shawulu, Kish da kuma Ner
mahaifin Abner, 'ya'yan Abiyel ne.
52 Dukan kwanakin Shawulu sun kasance na yaƙe-yaƙe da Filistiyawa ne. Duk
lokacin da Shawulu ya ga ƙaƙƙarfan mutum ko jarumi, sai yă ɗauke shi aikin sojansa.

# 15

### *Ubangiji ya ƙi Shawulu a matsayin sarki*

1 Sama'ila ya ce wa Shawulu, "Ni ne wanda Ubangiji ya aika in shafe ka ka zama
sarki bisa mutanensa Isra'ila. Saurara yanzu ka ji saƙo daga wurin Ubangiji. 2 Ga
abin da Ubangiji Maɗaukaki ya ce, 'Zan hori Amalekawa saboda abin da suka yi wa
Isra'ila sa'ad da suka ba su wahala yayinda suka fito daga Masar. 3 Yanzu ka tafi ka
yaƙi Amalekawa, ka hallaka kome da yake nasu, kada ka bar su da rai, ka kashe maza,
da mata, da yara, da jarirai, da dabbobi, da tumaki, da raƙuma, da kuma jakuna.' "
4 Sai Shawulu ya tattara sojoji, ya ƙidaya su a Telayim, ya sami su dubu ɗari biyu
da dubu goma daga Yahuda. 5 Shawulu ya tafi birnin Amalek ya yi kwanto a kwari.
6 Sai Shawulu ya ce wa Keniyawa, "Ku tashi ku bar Amalekawa don kada in hallaka
ku tare da su, saboda kun yi wa dukan Isra'ilawa kirki, lokacin da suka fito daga
Masar." Saboda haka Keniyawa suka tashi suka bar Amalekawa.
7 Sa'an nan Shawulu ya ci Amalekawa da yaƙi tun daga Hawila har zuwa Shur, a
gabashin iyakar Masar. 8 Ya kama Agag sarkin Amalekawa da rai. Ya kuma hallaka
dukan mutanensa da takobi. 9 Amma Shawulu da sojojinsa suka bar Agag, da tumaki,
da shanu, da 'yan maruƙa masu ƙiba da kuma duk abin da yake mai kyau da rai.
Waɗannan ba su so su hallaka su gaba ɗaya ba, amma duk abin da ba a so da kuma
marar amfani suka hallaka.
10 Sai Ubangiji ya yi magana da Sama'ila ya ce, 11 "Na damu da na naɗa Shawulu
sarki, domin ya juya mini baya, bai kuma bi umarnina ba." Sama'ila ya damu ƙwarai,
ya yi kuka ga Ubangiji dukan dare.
12 Kashegari da sassafe sai Sama'ila ya tashi ya tafi domin yă sadu da Shawulu,
amma aka gaya masa cewa Shawulu ya tafi Karmel. A can ya yi wa kansa abin
tunawa don yă girmama kansa, daga can kuma ya juya ya gangara zuwa Gilgal.
13 Da Sama'ila ya kai wurinsa, sai Shawulu ya ce, "Ubangiji yă albarkace ka, na
aikata umarnin Ubangiji."
14 Amma Sama'ila ya ce, "Ashe, waɗannan ba kukan tumaki ke nan nake ji a
kunnena ba? Wane kuka shanu ke nan nake ji?"
15 Shawulu ya amsa ya ce, "Sojoji ne suka kawo su daga Amalekawa. Sun bar
tumaki da shanu masu kyau da rai don su yi wa Ubangiji Allahnka hadaya, amma
sauran mun hallaka duka."

16 Sama'ila ya ce, "Dakata, bari in faɗa maka abin da UBANGIJI ya ce mini jiya da
dare."
Shawulu ya ce, "Gaya mini."
17 Sama'ila ya ce, "Ko da yake kana ganin kanka kai ba wani abu ne ba, ashe, ba
kai ne yanzu shugaban kabilan Isra'ila ba? UBANGIJI ya shafe ka ka zama sarkin
Isra'ila. 18 Shi kuma ya aika, ya umarce ka cewa, 'Tafi ka hallaka Amalekawa
mugayen mutanen nan duka, ka yaƙe su sai ka share su ƙaf.' 19 Me ya sa ba ka
bi umarnin UBANGIJI ba? Me ya sa ka sa hannu a ganima, ka kuma yi mugun abu a
gaban UBANGIJI?"
20 Shawulu ya ce, "Amma na bi umarnin UBANGIJI. Na bi saƙon da UBANGIJI ya ba
ni. Na hallaka Amalekawa, na kuma kamo Agag sarkinsu. 21 Sojoji suka kawo tumaki
da shanu mafi kyau daga cikin ganimar domin a miƙa hadaya ga UBANGIJI Allahnka
a Gilgal."
22 Amma Sama'ila ya ce,
"UBANGIJI yana murna da sadaka da hadaya
fiye da biyayya ga maganar UBANGIJI?
Yin biyayya ta fi hadaya
a kula kuma ta fi ƙibabbun raguna.
23 Gama tawaye yana kama da zunubi na duba,
girman kai kuma yana kama da bautar gumaka.
Saboda ka ƙi maganar UBANGIJI,
shi ma ya ƙi ka da zaman sarki."
24 Sai Shawulu ya ce wa Sama'ila, "Na yi zunubi, na ƙi bin umarnin UBANGIJI, na
kuma ƙi bin maganarka. Na ji tsoron mutane ne shi ya sa na bi maganarsu. 25 Yanzu
fa, ina roƙonka ka yafe mini zunubina, ka koma tare da ni, domin in yi wa UBANGIJI
sujada."
26 Amma Sama'ila ya ce, "Ba zan koma tare da kai ba. Ka ƙi maganar UBANGIJI,
UBANGIJI kuma ya ƙi ka da zama sarki a bisa Isra'ila."
27 Da Sama'ila ya juya zai tafi, sai Shawulu ya kama bakin rigarsa, sai rigar ta yage.
28 Sama'ila ya ce masa, "UBANGIJI ya yage masarautar Isra'ila daga gare ka yau, ya
ba wa wani daga cikin maƙwabtanka wanda ya fi ka. 29 Shi wanda yake Ɗaukakar
Isra'ila ba ya ƙarya ko yǎ canja zuciyarsa, gama shi ba mutum ba ne da zai canja
zuciyarsa."
30 Shawulu ya ce, "Na yi zunubi. Amma ina roƙonka ka ba ni girma a gaban
dattawan mutanena da kuma a gaban Isra'ila, ka koma tare da ni domin in yi wa
UBANGIJI Allahnka sujada." 31 Saboda haka sai Sama'ila ya koma tare da Shawulu,
Shawulu kuwa ya yi wa UBANGIJI sujada.
32 Sa'an nan Sama'ila ya ce, "Kawo mini Agag sarkin Amalekawa."
Agag kuwa ya zo wurinsa daure da sarƙa,* yana tunani cewa, "Tabbatacce zancen
mutuwa dai ya wuce."
33 Amma Sama'ila ya ce,
"Yadda takobinka ya sa mata suka rasa 'ya'ya,
haka mahaifiyarka za tǎ zama marar 'ya'ya a cikin mata."
Sama'ila kuwa ya kashe Agag a Gilgal a gaban UBANGIJI.
34 Sai Sama'ila ya tafi Rama, amma Shawulu ya haura zuwa gidansa a Gibeya na
Shawulu. 35 Daga wannan rana Sama'ila bai ƙara saduwa da sarki Shawulu ba, har
rasuwar Sama'ila, amma ya yi baƙin ciki sosai a kan Shawulu. UBANGIJI kuwa ya
damu da ya sa Shawulu ya zama Sarkin Isra'ila ba.

* **15:32** Ko kuwa yana rawar jiki, duk da haka

# 16

*Sama'ila ya shafe Dawuda da mai*

1 UBANGIJI ya ce wa Sama'ila, "Har yaushe za ka yi ta makoki saboda Shawulu? Na
riga na ƙi shi da zaman sarkin Isra'ila. Ka cika ƙahonka da mai, zan aike ka zuwa
wurin Yesse na Betlehem. Na zaɓi ɗaya daga cikin 'ya'yansa maza yă zama sarki."
2 Amma Sama'ila ya ce, "Yaya zan yi haka? Ai, in Shawulu ya ji labari, zai kashe
ni."
UBANGIJI ya ce, "To, sai ka tafi tare da 'yar karsana ka ce, 'Na zo don in yi wa
UBANGIJI hadaya.' 3 Ka gayyato Yesse a wurin hadayar, ni kuma zan gaya maka abin
da za ka yi. Za ka shafe mini wanda na nuna maka."
4 Sama'ila kuwa ya yi abin da UBANGIJI ya umarce shi. Da ya isa Betlehem, sai
dattawan garin suka tarye shi da rawar jiki, suka ce masa, "Mai duba, wannan ziyara
lafiya dai ko?"
5 Sama'ila ya ce, "I, lafiya ƙalau. Na zo ne domin in yi wa UBANGIJI hadaya. Ku
tsarkake kanku sa'an nan ku zo mu tafi wurin yin hadaya tare." Ya kuma sa Yesse
da 'ya'yansa maza su tsarkake kansu, su je wurin hadayar.
6 Da isarsu, Sama'ila ya ga Eliyab sai ya yi tsammani shi ne, sai ya ce, "Lalle ga
shafaffe na UBANGIJI tsaye a gaban UBANGIJI."
7 Amma UBANGIJI ya ce wa Sama'ila, "Kada ka dubi kyan tsarinsa ko tsayinsa,
domin ba shi nake so ba, gama yadda UBANGIJI yake gani, ba haka mutum yake gani
ba. Mutum yakan dubi kyan tsari ne kawai daga waje, amma UBANGIJI yakan dubi
zuciya."
8 Sai Yesse ya kira Abinadab yă zo gaban Sama'ila. Amma Sama'ila ya ce, "Ko
wannan ma UBANGIJI bai zaɓe shi ba." 9 Sai Yesse ya sa Shamma yă zo gaban Sama'ila,
amma Sama'ila ya ce, "UBANGIJI bai zaɓi wannan ma ba." 10 Yesse ya sa 'ya'yansa
maza bakwai suka wuce gaban Sama'ila, amma Sama'ila ya ce masa, "UBANGIJI bai
zaɓi waɗannan ba." 11 Don haka ya tambayi Yesse ya ce, "Su ke nan 'ya'yan maza
da kake da su?"
Yesse ya ce, "Har yanzu akwai ɗan autan, amma yana kiwon tumaki."
Sama'ila ya ce, "Ka aika yă zo, ba za mu zauna ba sai ya iso."
12 Sai ya aika aka kawo shi. Ga shi kuwa kyakkyawan saurayi ne mai kyan gani.
UBANGIJI ya ce, "Tashi ka shafe shi, shi ne wannan."
13 Saboda haka Sama'ila ya ɗauko ƙahon nan da yake da mai ya shafe Dawuda a
gaban 'yan'uwansa. Daga wannan rana kuwa ruhun UBANGIJI ya sauko wa Dawuda
da iko. Sai Sama'ila ya koma Rama.

*Dawuda ya shiga yin wa Shawulu hidima*

14 To, fa, Ruhun UBANGIJI ya riga ya rabu da Shawulu, sai mugun ruhu daga UBANGIJI
ya soma ba shi wahala.
15 Ma'aikatan Shawulu suka ce masa, "Duba, ga mugun ruhu daga Allah yana ba
ka wahala. 16 Ranka yă daɗe, muna so ka ba mu izini mu tafi, mu nemo wanda ya
iya kiɗan molo, domin duk sa'ad da mugun ruhun nan daga Allah ya tashi, sai yă
kaɗa molon don hankalinka yă kwanta."
17 Saboda haka Shawulu ya ce wa ma'aikatansa, "Ku nemo wanda ya iya kiɗan
molo sosai ku kawo mini."
18 Ɗaya daga cikin bayin ya ce, "Na san wani yaro, ɗan Yesse na Betlehem, ya iya
kiɗan molo, yana da hikima, shi kuma ya iya yaƙi. Ya iya magana, ga shi kuma
kyakkyawa, UBANGIJI kuwa yana tare da shi."
19 Sai Shawulu ya aiki manzanni zuwa wurin Yesse ya ce, "Ka aiko mini da ɗanka
Dawuda wanda yake kiwon tumaki." 20 Saboda haka Yesse ya ɗauki jaki tare da

burodi da ruwan inabi da ɗan ƙarami bunsuru ya ba wa ɗansa Dawuda yă kai wa
Shawulu.
21 Dawuda ya isa wurin Shawulu ya shiga hidimarsa. Shawulu kuwa ya so shi
ƙwarai da gaske. Dawuda ya zama ɗaya daga cikin masu sanya sulke. 22 Saʼan nan
Shawulu ya aika saƙo wurin Yesse cewa, “Ka bar Dawuda yă yi mini hidima domin
ina jin daɗinsa ƙwarai.”
23 Duk lokacin da ruhun nan daga Allah ya sauko a kan Shawulu, sai Dawuda yă
ɗauki molonsa yă kaɗa. Saʼan nan sauƙi yă zo wa Shawulu, mugun ruhu kuma yă
rabu da shi.

# 17

*Dawuda da Goliyat*

1 To, fa, Filistiyawa suka tattara mayaƙansu suka haɗu a Soko cikin Yahuda domin
yaƙi. Suka yi sansani a Efes-Dammim, tsakanin Soko da Azeka. 2 Shawulu da
Israʼilawa suka taru suka yi sansani a Kwarin Ela suka ja dāgā don su yi yaƙi da
Filistiyawa. 3 Filistiyawa suka zauna a tudu guda, Israʼilawa kuma suka zauna a
ɗaya tudun. Kwari yana a tsakaninsu.
4 Wani jarumin da ake kira Goliyat wanda ya fito daga Gat, ya fita daga sansanin
Filistiyawa. Tsawonsa ya fi ƙafa tara. 5 Ya sa hular kwanon da aka yi da tagulla, da
rigar ƙarfe mai sulke, nauyin rigar ya kai shekel dubu biyar. 6 A ƙafafunsa kuwa
ya sa ƙarafar tagulla, rataye a bayansa kuma māshi ne na tagulla. 7 Kotar kibiyarsa
kuwa kamar sandar saƙar igiya take, ƙarfen kibiyar kuma nauyinsa ya kai shekel
ɗari shida. Mai riƙe masa garkuwa yana tafe a gabansa.
8 Goliyat ya tsaya ya tā da murya wa hafsoshin Israʼila ya ce, “Me ya sa kuka fito
kuna layi don yaƙi? Ni ba Bafilistin ba ne? Ku kuma ba bayin Shawulu ba ne? Ku zaɓi
waninku yă zo nan. 9 In zai iya yin faɗa har yă kashe ni, to, za mu zama bayinku.
Amma in na fi ƙarfinsa na kashe shi, to, sai ku zama bayinmu, ku kuma yi mana
bauta.” 10 Sai Bafilistin ya ce, “A wannan rana, na kalubalanci sojojin Israʼila, ku ba
ni mutum ɗaya mu yi faɗa.” 11 Da jin maganganun Bafilistin, sai Shawulu da dukan
Israʼila suka damu suka kuma ji tsoro.
12 To, Dawuda dai ɗan wani mutumin Efratawa ne mai suna Yesse, shi mutumin
Betlehem ne a cikin Yahudiya. Yesse yana da yara maza takwas, a zamanin Shawulu
kuwa, Yesse ya riga ya tsufa. 13 Manyan ʼyaʼyansa maza uku, sun bi Shawulu wajen
yaƙi. Ɗansa na fari shi ne Eliyab, na biyu shi ne Abinadab, na uku kuwa shi ne
Shamma.
14 Dawuda shi ne ɗan autansu. Manyan ʼyan mazan nan uku suka bi Shawulu.
15 Amma Dawuda yakan tafi sansanin Shawulu lokaci-lokaci yă kuma koma Betlehem
don yă yi kiwon tumakin mahaifinsa.
16 Kwana arbaʼin cif, Bafilistin nan ya yi ta fitowa kowane safe da kuma kowace
yamma.
17 Yesse ya ce wa ɗansa Dawuda, “Ka ɗauki wannan gasasshen hatsi da waɗannan
curin burodi goma, ka kai wa ʼyanʼuwanka a sansani da sauri. 18 Ka haɗa da
waɗannan cuku guda goma, ka kai wa komandan rundunarsu. Ka ga lafiyar
ʼyanʼuwanka, ka kawo mini labari daga wurinsu. 19 Suna tare da Shawulu da kuma
dukan mutanen Israʼila a Kwarin Ela, suna can suna yaƙi da Filistiyawa.”
20 Kashegari da sassafe, Dawuda ya tashi ya bar tumakinsa wa wani yă lura da
su, sai ya ɗauki kayansa, ya kama hanya kamar yadda Yesse ya umarce shi. Ya
isa sansanin daidai saʼad da rundunar tana fitowa zuwa bakin dāgā, suna kirarin
yaƙi. 21 Israʼila da Filistiyawa suka ja dāgā suna fuskantar junansu. 22 Dawuda ya
bar kayansa a wajen wani mai lura da kaya, sai ya ruga zuwa bakin dāgā yă gai da

'yan'uwansa. 23 Da yana magana da su sai Goliyat, jarumin nan Bafilistin daga Gat ya
fito daga rundunar Filistiyawa, ya tā da murya kamar yadda ya saba. Dawuda kuwa
ya ji shi. 24 Da Isra'ilawa suka ga mutumin, sai dukansu suka gudu saboda tsananin
tsoro.
25 Isra'ilawa suka yi ta cewa, "Kun ga yadda wannan mutum yana ta fitowa? Yana
fitowa ne don yă kalubalanci Isra'ila. Sarki zai sāka wa mutumin da ya kashe wannan
da dukiya mai yawa. Zai kuma ba shi 'yarsa yă aura, yă cire suna mahaifinsa daga
biyan kuɗin haraji cikin Isra'ila."
26 Dawuda ya tambayi mutanen da suke tsaye kusa da shi ya ce, "Me za a yi wa
wanda ya kashe Bafilistin nan, ya kuma cire wannan kunya daga Isra'ila? Wane ne
wannan bafilistin marar kaciya da yake kalubalantar rundunar yaƙi na Allah mai
rai?"
27 Sai suka sāke gaya masa abin da suka faɗa cewa, "Ga abin da zai faru da wanda
ya kashe shi."
28 Da wansa Eliyab, ya ji yana magana da mutanen, sai ransa ya ɓace ƙwarai saboda
fushi, sai ya ce wa Dawuda, "Me ka zo yi a nan? Wa kuma ka bar wa 'yan tumakin
a jeji? Na san ka da taurinkai, da kuma mugun hali. Ka zo nan ne don ka yi kallon
yaƙi kawai."
29 Dawuda ya ce, "To, yanzu me na yi? Ba zan ma yi magana ba?" 30 Sai ya juya
wajen wani kuma ya sāke kawo zancen, mutanen kuwa suka amsa masa kamar dā.
31 Aka ji abin da Dawuda ya ce, aka kuwa gaya wa Shawulu, Shawulu kuma ya aika
a kawo shi.
32 Da Shawulu ya tambayi Dawuda, sai Dawuda ya ce masa, "Kada kowa yă damu
saboda wannan Bafilistin. Bawanka zai je yă yi faɗa da shi."
33 Shawulu ya ce, "Ba za ka iya yin faɗa da wannan Bafilistin ba, ya daɗe yana
yaƙi, ya yi yaƙi tun yana saurayi. Ga shi kuwa kai ɗan yaro ne kawai."
34 Amma Dawuda ya ce wa Shawulu, "Bawanka yana kiwon tumakin mahaifinsa.
Sa'ad da zaki ko beyar ta zo ta kama tunkiya, ta tafi da ita. 35 Nakan bi ta a baya in
buga ta in kuma ƙwato tunkiyar daga bakinta. In kuma ta taso mini, nakan cafke ta
a gashinta in buga ta in kashe. 36 Bawanka ya kashe zaki da beyar, wannan Bafilistin
marar kaciya zai zama kamar ɗaya daga cikinsu, domin ya rena rundunar Allah mai
rai. 37 Ubangiji wanda ya cece ni daga kumbar zaki da kuma kumbar beyar, zai cece
ni daga hannun wannan Bafilistin."
Shawulu ya ce wa Dawuda, "Je ka, Ubangiji yă kasance tare da kai."
38 Sai Shawulu ya kawo kayan yaƙinsa ya sa wa Dawuda. Ya sa masa hular kwanon
da aka yi da tagulla a kansa, ya kuma sa masa rigar ƙarfensa. 39 Dawuda ya ɗaura
māshin Shawulu a sulken, ya yi ƙoƙari yă zaga, sai ya ji ba zai iya ba saboda bai saba
ba.
Ya cewa Shawulu, "Ba zan iya tafiya da waɗannan ba, domin ban saba ba." Don
haka ya tuɓe su. 40 Sai ya ɗauki sandansa, ya zaɓi duwatsu guda biyar masu sulɓi
daga cikin rafi, ya sa su a 'yar jakarsa ta makiyaya; ya kuma ɗauki majajjawarsa, ya
tafi, yă fuskanci Bafilistin.
41 Ana ciki haka, sai Bafilistin nan shi ma ya fita yana gusowa zuwa wurin Dawuda.
Mai riƙe masa garkuwar yaƙi kuwa yana tafe a gabansa. 42 Bafilistin ya dubi Dawuda
daga sama har ƙasa, ya gan dai ɗan yaro ne kawai, kyakkyawa kuma mai ƙoshin
lafiya, sai ya rena shi. 43 Ya ce masa, "Kana tsammani ni kare ne da za ka zo mini da
sanda?" Sai ya la'anci Dawuda da sunayen allolin Filistiyawa. 44 Ya ce, "Zo nan, ni
kuwa zan ba da naman jikinka ga tsuntsayen sama da namun jeji su ci."
45 Dawuda ya ce wa Bafilistin, "Kana zuwa ka yaƙe ni da māshi da takobi da kere,
amma ni ina zuwa in yaƙe ka a cikin sunan Ubangiji Maɗaukaki, Allah na rundunar
Isra'ila, wanda ka rena. 46 Yau nan, Ubangiji zai bashe ka a hannuna, zan kuwa kashe

ka, in datse kanka. Yau, zan ba da gawawwakin rundunar Filistiyawa ga tsuntsayen
sama da namun jeji, da haka duniya za tă sani lalle akwai Allah a cikin Isra'ila. 47 Duk
waɗanda suka taru a nan za su san cewa ba da māshi ko takobi ne UBANGIJI yake ceto
ba, gama yaƙin nan na UBANGIJI ne, shi kuwa zai bashe ku duka a hannuwanmu."
48 Yayinda Bafilistin yana matsowa kusa domin yă fāɗa wa Dawuda, sai Dawuda
ya ruga a guje zuwa bakin dāgā don yă same shi. 49 Ya sa hannu a jakarsa ya ɗauki
dutse, ya sa cikin majajjawa ya wurga, dutsen kuwa ya bugi Bafilistin a goshi, dutsen
ya shiga cikin goshinsa, sai Bafilistin ya fāɗi rubda ciki.
50 Da majajjawa da dutse kawai Dawuda ya ci nasara a kan Bafilistin. Ya buge shi,
ya kashe shi ba tare da takobi a hannunsa ba.
51 Dawuda ya ruga ya tsaya a bisan Bafilistin, ya zare takobin Bafilistin daga
kubensa, ya datse masa kai da shi.
Da Filistiyawa suka ga jaruminsu ya mutu, sai suka juya suka gudu. 52 Mutanen
Isra'ila da na Yahuda suka rugo gaba da babbar murya, suka fafari Filistiyawa har
zuwa mashigin Gat da kuma ƙofofin Ekron. Gawawwakin Filistiyawa suka bazu a
hanyar Sha'arayim zuwa Gat da kuma Ekron. 53 Da Isra'ilawa suka komo daga bin
Filistiyawa sai suka washe sansanin Filistiyawa.
54 Dawuda ya ɗauki kan Bafilistin zuwa Urushalima. Sai Dawuda ya ajiye kayan
yaƙin Bafilistin a tentinsa.
55 Yayinda Shawulu yake kallon Dawuda sa'ad da za shi yă yaƙi Bafilistin, sai ya
tambayi Abner, komandan rundunarsa ya ce, "Abner, ɗan wane ne wannan saurayi?"
Abner ya ce ran sarki yă daɗe, "Ban sani ba."
56 Sarki ya ce, "Ka tambaya mini ko yaron wane ne wannan saurayi."
57 Dawuda yana dawowa daga karkashe Filistiyawa ke nan, sai Abner ya kai shi
gaban Shawulu, riƙe da kan Bafilistin.
58 Sai Shawulu ya ce, "Kai ɗan wane ne, saurayi?"
Dawuda ya ce, "Ni ɗan bawanka Yesse ne, na Betlehem."

# 18

*Shawulu ya fara kishin Dawuda*

1 Bayan da Dawuda ya gama magana da Shawulu, sai Yonatan ɗan Shawulu ya ji
zuciyarsa tana son Dawuda sosai. Yonatan kuwa yana ƙaunar Dawuda kamar ransa.
2 Tun daga wannan rana Shawulu ya zaunar da Dawuda tare da shi, bai bar shi ya
koma gidan mahaifinsa ba. 3 Yonatan kuma ya yi yarjejjeniya da Dawuda saboda
yana ƙaunarsa kamar ransa. 4 Yonatan ya tuɓe doguwar taguwarsa da ya sa, ya ba
wa Dawuda, tare da sulkensa, har ma da māshi da kibiyarsa, da kuma bel nasa.
5 Duk abin da Shawulu ya aiki Dawuda yă yi yakan yi shi cikin aminci, har Shawulu
ya ba shi babban makami a rundunarsa. Wannan ya faranta wa dukan mutane zuciya
har ma da ma'aikatan Shawulu.
6 Yayinda mutane suke dawowa gida bayan da Dawuda ya kashe Bafilistin, mata
suka fito daga dukan biranen Isra'ila don su sadu da Sarki Shawulu, suna waƙoƙi da
raye-raye masu farin ciki, da ganguna da sarewa. 7 Suna rawa suna cewa,
"Shawulu ya kashe dubbansa,
Dawuda kuwa ya kashe dubun dubbai."
8 Shawulu kuwa ya ji fushi, wannan magana ba tă yi masa daɗi ba, ya yi tunani ya
ce, "Suna yabon Dawuda cewa ya kashe dubun dubbai amma ni dubbai kawai. Me
ya rage masa yanzu, in ba mulki ba?" 9 Tun daga wannan lokaci zuwa gaba, Shawulu
ya dinga kishin Dawuda.
10 Kashegari, mugun ruhu daga Allah ya fāɗo wa Shawulu da tsanani. Yana annabci
a gidansa, Dawuda kuwa yana bugan molo kamar yadda ya saba. Shawulu yana riƙe

da māshi a hannunsa. [11] Da ƙarfi yana magana da kansa yana cewa, "Zan kafe
Dawuda da bango." Amma Dawuda ya bauɗe masa sau biyu.

[12] Shawulu ya ji tsoron Dawuda don UBANGIJI yana tare da shi, amma UBANGIJI ya
riga ya bar Shawulu. [13] Saboda haka Shawulu bai yarda Dawuda yă zauna tare da
shi ba, amma ya maishe shi shugaban sojoji dubu. Dawuda kuwa ya riƙa bi da su
yana kaiwa yana kuma da tare da su.

### *Dawuda ya bi da runduna a yaƙe-yaƙensu*

[14] A kome da Dawuda ya yi yakan yi nasara gama UBANGIJI yana tare da shi. [15] Da
Shawulu ya ga yadda yake cin nasara, sai ya ji tsoronsa. [16] Amma dukan Isra'ila da
Yahuda suka ƙaunaci Dawuda gama yana bin da su a yaƙe-yaƙensu.

[17] Shawulu ya ce wa Dawuda, "Ga diyata Merab zan ba ka ka aura, kai dai ka yi
mini aiki da himma, ka kuma yi yaƙe-yaƙen UBANGIJI." Saboda Shawulu ya ce wa
kansa, "Ba zan ɗaga hannuna a kansa ba, Filistiyawa ne za su yi wannan."

[18] Amma Dawuda ya ce wa Shawulu, "Wane ni, wa ya san iyayena ko kabilar
iyayena a Isra'ila da zan zama surukin sarki?" [19] Da lokaci ya kai da Merab 'yar
Shawulu za tă yi aure da Dawuda, sai aka aurar da ita wa Adriyel na Mehola.

[20] Mikal 'yar Shawulu kuwa tana ƙaunar Dawuda sosai. Da aka gaya wa Shawulu
labarin, sai ya yi farin ciki, ya yi tunani ya ce, [21] "Zan ba shi ita tă zama masa tarko,
da haka Filistiyawa za su same shi." Shawulu ya ce wa Dawuda, "Yanzu kana da
dama sau na biyu ka zama surukina."

[22] Sai Shawulu ya umarci ma'aikatansa cewa, "Ku yi magana da Dawuda asirce
ku ce, 'Duba, sarki yana farin ciki da kai, dukan ma'aikatansa kuma suna sonka, ka
yarda ka zama surukinsa.' "

[23] Suka sāke yi wa Dawuda wannan magana amma Dawuda ya ce, "Kuna tsammani
abu mai sauƙi ne mutum yă zama surukin sarki? Ni talaka ne, kuma ba sananne ba."

[24] Da ma'aikatan Shawulu suka gaya masa abin da Dawuda ya faɗa. [25] Sai Shawulu
ya ce, "Ku gaya wa Dawuda, 'Sarki ba ya bukatan kuɗin auren 'yarsa, sai dai loɓar
Filistiyawa domin ramako a kan abokan gābansa.' " Shawulu yana shiri ne domin
Dawuda yă fāɗa a hannun Filistiyawa.

[26] Da ma'aikatan suka gaya wa Dawuda waɗannan abubuwa, sai ya yi murna don
zai zama surukin sarki. Amma kafin lokacin yă cika, [27] Dawuda da mutanensa suka
fita suka kashe Filistiyawa ɗari biyu, suka kawo loɓar suka miƙa wa sarki, domin yă
zama surukin sarki. Sai Shawulu ya ba da 'yarsa Mikal aure ga Dawuda.

[28] Da Shawulu ya gane UBANGIJI yana tare da Dawuda, 'yarsa Mikal kuma tana
ƙaunarsa, [29] sai Shawulu ya ƙara jin tsoron Dawuda har ya zama maƙiyinsa a dukan
sauran rayuwarsa.

[30] Manyan sojojin Filistiyawa suka yi ta fita suna yaƙi da Isra'ilawa, amma kullum
Dawuda yakan sami nasara fiye da sauran manyan sojojin Shawulu. Ta haka ya yi
suna ƙwarai.

## 19

### *Shawulu ya yi ƙoƙari yă kashe Dawuda*

[1] Shawulu ya gaya wa ɗansa Yonatan da ma'aikatansa su kashe Dawuda. Amma
Yonatan yana son Dawuda sosai. [2] Sai ya gargaɗe shi ya ce, "Mahaifina Shawulu yana
neman hanyar da zai kashe ka. Ka kula da kanka gobe da safe, ka tafi wani wuri ka
ɓuya. [3] Zan je in tsaya da mahaifina a fili inda kake, zan yi masa magana game da
kai. Zan kuma gaya maka abin da na ji."

[4] Yonatan ya yi magana mai kyau a kan Dawuda a wajen mahaifinsa ya ce, "Kada
sarki yă yi wani mummunan abu wa bawansa Dawuda, gama bai yi maka wani abu

marar kyau ba. Abin da ya yi ya amfane ka ƙwarai da gaske. [5] Ya yi kasai da ransa
sa'ad da ya kashe Bafilistin nan. UBANGIJI ya ba wa dukan Isra'ila babban nasara,
ka gani, ka kuma yi farin ciki. Don me za ka ci mutuncin amintaccen mutum kamar
Dawuda ta wurin kashe shi ba tare da wani dalili ba?"

[6] Shawulu ya saurari Yonatan sai ya rantse ya ce, "Muddin UBANGIJI yana a raye,
ba za a kashe Dawuda ba."

[7] Ta haka Yonatan ya kira Dawuda ya gaya masa dukan maganarsu. Ya kawo shi
wurin Shawulu, Dawuda kuwa ya zauna tare da Shawulu kamar dā.

[8] Wani yaƙi ya sāke tashi, Dawuda kuwa ya fita ya yaƙi Filistiyawa, ya kai musu
hari mai tsanani, sai da suka gudu a gabansa.

[9] Amma mugun ruhu daga UBANGIJI ya sauko wa Shawulu yayinda yana zaune a
cikin gidansa da māshi a hannunsa. Yayinda Dawuda yake bugan molo, [10] Shawulu
ya yi ƙoƙari yă kafe shi da bango da māshinsa, amma Dawuda ya goce sa'ad da
Shawulu jefa māshin a bango. A daren nan Dawuda ya nemi hanya ya gudu.

[11] Shawulu ya aiki mutane zuwa gidan Dawuda su yi gadin gidan, su kuma kashe
Dawuda. Amma Mikal matar Dawuda ta gargaɗe Dawuda, ta ce, "In ba ka gudu a
daren nan ba, kashegari za a kashe ka." [12] Haka kuwa Mikal ta sauko da Dawuda ta
taga ya gudu, ya tsere. [13] Sai Mikal ta ɗauki gunki ta kwantar da shi a gādo, ta sa
masa gashin akuya a kansa, sai ta rufe da mayafi.

[14] Da Shawulu ya aiki mutane su kama Dawuda. Mikal ta ce, "Ba shi da lafiya."

[15] Sai Shawulu ya sāke aiki mutanen su ga Dawuda, ya ce musu, "Ku kawo shi a
gādonsa domin in kashe shi." [16] Amma da mutanen suka shiga sai suka ga gunkin a
gadon, a wajen kan kuwa akwai gashin akuya.

[17] Shawulu ya ce wa Mikal, "Don me kika ruɗe ni har kika bar maƙiyina ya gudu
ya tsere?"

Mikal ta ce masa, "Ya ce mini, 'Idan ban bar shi ya tafi ba, zai kashe ni?' "

[18] Da Dawuda ya gudu ya tsere, sai ya tafi wurin Sama'ila a Rama ya gaya masa
dukan abin da Shawulu ya yi masa. Da shi da Sama'ila suka tafi Nayiwot suka zauna
a can. [19] Shawulu ya sami labari cewa, "Dawuda yana Nayiwot a Rama." [20] Sai ya aiki
mutane su je su kamo Dawuda, amma da suka ga ƙungiyar annabawa suna annabci
tare da Sama'ila shugabansu a tsaye, sai Ruhun Allah ya sauko wa mutanen Shawulu,
su ma suka fara yin annabci. [21] Shawulu ya sami labari game da wannan, sai ya sāke
aiken waɗansu da yawa. Su ma suka shiga yin annabci. Shawulu ya sāke aiken
mutane sau na uku, su kuma suka shiga yin annabci. [22] A ƙarshe, shi da kansa ya
tashi ya tafi Rama. Ya bi ta babban rijiyar ruwan Seku. A can ya yi tambaya ya ce,
"Ina Sama'ila da Dawuda suke?"

Suka ce, "Suna cikin Nayiwot a Rama."

[23] Saboda haka Shawulu ya tafi Nayiwot a Rama, amma Ruhun Allah ya sauko masa,
shi ma ya yi tafiya yana annabci har sai da ya isa Nayiwot. [24] Ya tuttuɓe rigunarsa,
ya kuma yi annabci a gaban Sama'ila. Ya kwanta tsirara dukan yini da dukan dare.
Abin da ya sa ke nan mutane suke cewa, "Shawulu ma yana cikin annabawa ne?"

# 20

*Dawuda da Yonatan*

[1] Sai Dawuda ya gudu daga Nayiwot a Rama ya je wurin Yonatan ya ce, "Me na yi?
Wane laifi ne na yi? Ta wace hanya ce na yi wa mahaifinka laifi har da yake neman
yă kashe ni?"

[2] Yonatan ya ce, "Faufau, ba za ka mutu ba! Ka ji nan, mahaifina ba ya yin kome
ba tare da ya shawarce da ni ba. Me ya sa ya ɓoye mini wannan? Ba zai yiwu ba."

3 Sai Dawuda ya rantse ya ce, "Mahaifinka ya san cewa, na sami tagomashi a gare
ka, domin haka ba zai sanar maka da wannan ba, don kada yă baƙanta maka rai. Na
rantse da Ubangiji, da kai kuma, taki ɗaya kaɗai ya rage tsakanina da mutuwa."

4 Sai Yonatan ya ce, "Duk abin da kake so in yi maka zan yi."

5 Dawuda ya ce, "Gobe fa shi ne Bikin Sabon Wata, ya kamata in ci tare da sarki
amma bari in tafi fili in ɓuya har jibi da yamma. 6 In mahaifinka bai gan ni ba,
ka gaya masa cewa, 'Dawuda ya nemi izinina domin yă hanzarta yă tafi garinsa a
Betlehem saboda ana hadaya ta shekara-shekara don dukan zuriyarsa.' 7 In ya yi
na'am, to, bawanka ya tsira. Amma in ka ga ya damu, to, ka tabbata ya yi niyya yă
kashe ni. 8 Kai kuma, ka nuna alheri ga bawanka, gama ka riga ka yi yarjejjeniya da
ni a gaban Ubangiji, in kuwa na yi laifi ne sai ka kashe ni da kanka. Don me za ka
bashe ni ga mahaifinka?"

9 Yonatan ya ce, "Labudda! In na ji ƙishin-ƙishin, cewa mahaifina yana neman yă
kashe ka ashe, ba zan gaya maka ba?"

10 Dawuda ya ce, "Wa zai gaya mini idan mahaifinka ya amsa maka da amsa marar
daɗi?"
11 Yonatan ya ce, "Zo mu fita zuwa fili." Sai suka tafi tare.

12 Sai Yonatan ya ce wa Dawuda, "Na yi rantse da Ubangiji, Allah na Isra'ila cewa
war haka jibi, zan yi ƙoƙari in ji daga mahaifina, idan ya yi magana mai kyau game
da kai, zan gaya maka. 13 Amma in mahaifina ya sa zuciya yă cuce ka, Ubangiji yă
hukunta ni da hukunci mai tsanani in ban gaya maka ba, in kuma sa ka ka tafi lafiya.
Ubangiji yă kasance tare da kai kamar yadda ya kasance da mahaifina. 14 Amma ka
nuna mini alheri marar ƙarewa iri ta Ubangiji dukan rayuwata don kada a kashe ni.
15 Kada kuma ka yanke alherinka ga iyalina ko da Ubangiji ya hallaka dukan maƙiyin
Dawuda a duniya."

16 Saboda haka Yonatan ya yi yarjejjeniya da gidan Dawuda cewa Ubangiji yă kawo
dukan maƙiyin Dawuda ga mutuwa. 17 Yonatan kuwa ya sa Dawuda ya sāke tabbatar
masa rantsuwansa game da abokantakarsa da shi, gama yana ƙaunar Dawuda kamar
ransa.
18 Sai Yonatan ya gaya wa Dawuda cewa, "Gobe ne Bikin Sabon Wata, za a rasa ka,
da yake kujerarka za tă kasance ba kowa a kai. 19 Jibi wajajen yamma, ka tafi wurin
da ka ɓuya lokacin da wannan matsala ta fara, ka tsaya kusa da dutsen Etsel. 20 Zan
harbi kibiya uku ta wajen, sai ka ce dai ina harbin baka. 21 Sa'an nan zan aiki yaro in
ce masa, 'Je ka nemo kibiyoyin.' In na ce masa, 'Duba, kibiyoyin suna wannan gefen
da kake, kawo su,' sai ka fito, wato, tabbatacce muddin Ubangiji yana raye, ka tsira,
ba wani hatsari. 22 Amma in na ce wa yaron, 'Duba, kibiyoyin suna gaba da kai,' sai
ka tafi, gama Ubangiji ya sallame ka. 23 Game da al'amarin da muka tattauna da ni
da kai kuwa, ka tuna fa Ubangiji ne shaida tsakanina da kai har abada."

24 Dawuda ya tafi ya ɓuya a fili. Sa'ad da ranar Bikin Sabon Wata ta zo, sarki ya
zauna don yă ci. 25 Ya zauna a kujeransa inda ya saba zama kusa da bango yana
fuskantar Yonatan, Abner kuma ya zauna kusa da sarki. Amma kujeran Dawuda ba
kowa. 26 Shawulu bai ce kome ba a ranar domin ya yi tsammani wataƙila wani abu
ya faru da Dawuda ya mai da shi marar tsarki, tabbatacce ba shi da tsarki. 27 Amma
kashegari, rana ta biyu ga wata, kujeran Dawuda kuma ba kowa, sai Shawulu ya ce
wa ɗansa Yonatan, "Me ya sa ɗan Yesse bai zo cin abinci, jiya da yau ba?"

28 Yonatan ya ce, "Dawuda ya nemi izinina don yă tafi Betlehem. 29 Ya ce, 'Bari
in tafi gama iyalinmu suna miƙa hadaya a gari, 'yan'uwana kuwa sun gayyace ni in
kasance a can. In na sami yardarka, bari in tafi in ga 'yan'uwana.' Dalilin ke nan da
bai zo ci da sarki ba."

30 Fushin Shawulu ya ƙuna a kan Yonatan, sai ya ce masa, "Kai shege ne, haihuwar
banzan mace; ai, na san kana goyon bayan ɗan Yesse don ka wulaƙantar da kanka da
mahaifinka. 31 Muddin ɗan Yesse yana da rai a duniya, ba za ka kahu ba. Sarautarka
kuma ba za tă kahu ba. Yanzu sai ka je ka kawo mini shi. Dole yă mutu."
32 Yonatan ya ce wa mahaifinsa, "Me ya sa zai mutu? Me ya yi?" 33 Amma Shawulu
ya jefe shi da māshi don yă kashe shi. A nan ne Yonatan ya san lalle mahaifinsa ya
yi niyya yă kashe Dawuda.
34 Yonatan ya tashi daga tebur cin abincin da fushi. A rana ta biyun kuwa bai ci
abinci ba, gama yana baƙin ciki game da rashin kunyar mahaifinsa game da Dawuda.
35 Da safe Yonatan ya tafi domin yă sadu da Dawuda a fili. Ya tafi tare da wani
ƙaramin yaro. 36 Ya ce wa yaron, "Yi ruga da gudu ka nemo kibiyoyin da na harba."
Da yaron ya ruga sai ya harba kibiya a gaba da shi. 37 Da yaron ya isa wurin da
kibiyan Yonatan ya fāɗi, Yonatan ya kira shi ya ce, "Kibiyan na gabanka fa." 38 Sai ya
tā da murya ya ce, "Maza, yi sauri kada ka tsaya." Yaron ya ɗauko kibiya ya kawo
wa maigidansa. 39 (Yaron kuwa bai san kome game da wannan abu ba, sai Yonatan
da Dawuda kawai.) 40 Yonatan ya ba wa yaron makaman ya ce, "Ka ɗauka ka koma
gari."
41 Da yaron ya tafi, sai Dawuda ya tashi daga inda ya ɓuya kusa da tarin duwatsu,
ya rusuna har sau uku. Sa'an nan suka sumbaci juna, suka yi kuka, Dawuda kuwa
ya yi kuka sosai.
42 Yonatan ya ce wa Dawuda, "Sauka lafiya, mun riga mun yi rantsuwar abokantaka
da juna a cikin sunan UBANGIJI cewa, 'UBANGIJI ne shaida tsakanina da kai, tsakanin
zuriyarka da zuriyata har abada.' " Sai Dawuda ya tafi, Yonatan kuwa ya koma gari.

# 21

*Dawuda a Nob*

1 Dawuda ya tafi Nob a wurin Ahimelek firist. Da Ahimelek ya gan shi sai ya firgita
ya ce, "Me ya sa kai kaɗai ne? Me ya sa ba wani tare da kai?"
2 Dawuda ya ce wa Ahimelek firist, "Na zo aikin sarki ne, ya kuwa ce kada in sanar
wa kowa abin da ya sa in yi. Na faɗa wa mutanena inda za su same ni. 3 Yanzu, me
kake da shi a hannu? Ka ba ni burodi guda biyar, ko wani abu da kake da shi a nan."
4 Amma firist ya ce wa Dawuda, "Ba ni da burodi iri na kowa da kowa, sai dai
akwai burodin da aka tsarkake. Za ka iya ɗauka ku ci idan mutanenka ba su kwana
da mata ba."
5 Dawuda ya ce, "Lalle ne a keɓe muke daga mata. Mutanena sukan keɓe kansu a
koyaushe suka tashi 'yar tafiya, balle fa a yau!" 6 Don haka firist ya ba shi keɓaɓɓen
burodi, tun da yake babu wani burodi a can sai dai burodin Kasancewa da aka cire
daga gaban UBANGIJI, aka sa burodi mai zafi a maimakon wanda aka cire a ranar.
7 A ranar kuwa, ɗaya daga cikin bayin Shawulu yana can, a tsare a gaban UBANGIJI,
sunansa Doyeg, mutumin Edom, shugaban makiyayan Shawulu.
8 Dawuda ya ce wa Ahimelek, "Ba ka da māshi ko takobi a nan? Ban kawo māshina
ko wani makami ba gama saƙon sarki ya zo mini da gaggawa."
9 Sai firist ya ce, "Takobin Goliyat Bafilistin nan wanda ka kashe a Kwarin Ela yana
nan. An naɗe shi da ƙyallen aka ajiye a bayan Efod, in kana so, sai ka ɗauka. Ba
wani takobi kuma sai wancan."
Dawuda ya ce, "Ba ni shi, ai, ba wani kamar sa."

*Dawuda a Gat*

10 A ranar, Dawuda ya gudu daga wajen Shawulu ya tafi wuri Akish sarkin Gat.
11 Amma bayin Akish suka ce masa, "Wannan ba shi ne Dawuda sarkin ƙasar ba?
Ashe, ba shi ne aka yi ta yin waƙoƙi a kansa, ana raye-raye, ana cewa,

"Shawulu ya kashe dubbai,
Dawuda kuwa ya kashe dubun dubbai?"

12 Dawuda ya riƙe waɗannan kalmomi a zuciyarsa, ya kuma ji tsoron Akish sarkin
Gat sosai. 13 Don haka sai ya yi kamar ya taɓu a gabansu. A duk lokacin da yake tare
da su, sai yă yi kamar ya haukace. Ya yi ta zāne-zāne a ƙofofi*,* ya bar miyau yana ta
bin gemunsa.

14 Akish ya ce wa bayinsa, "Duba, wannan mutum yana hauka. Me ya sa kuka
kawo shi a wurina? 15 Na rasa masu hauka ne da za ku kawo mini wannan mutum
yă yi ta hauka a gabana? Dole ne wannan mutum yă shiga gidana?"

# 22

### *Dawuda a Adullam da Mizfa*

1 Dawuda ya bar Gat, ya tsere zuwa kogon Adullam. Da 'yan'uwansa da kuma
iyalan mahaifinsa suka ji labari, sai suka tafi can wurinsa. 2 Dukan mutanen da suke
cikin wahala, da waɗanda ake binsu bashi, da masu damuwoyi, suka tattaru a wurin
Dawuda. Shi kuwa ya zama shugabansu. Yawansu ya kai ɗari huɗu.

3 Daga can Dawuda ya tafi Mizfa a Mowab. Ya ce wa sarkin Mowab, "Za ka yarda
mahaifina da mahaifiyata su zo su zauna a wurinka kafin in san abin da Allah zai
yi da ni?" 4 Saboda haka ya bar su a wurin sarkin Mowab, suka zauna da shi duk
tsawon lokacin da Dawuda yake ta ɓuya a kogwannin duwatsu.

5 Amma annabin nan Gad ya ce wa Dawuda, "Kada ka zauna a nan, maza ka tashi
ka shiga ƙasar Yahuda". Sai Dawuda ya tashi ya tafi jejin Heret.

### *Shawulu ya kashe firistocin Nob*

6 Sai Shawulu ya sami labari cewa an ga Dawuda da mutanensa. Shawulu kuwa
yana zaune da māshinsa kusa a ƙarƙashin itacen tsamiya a tudun Gibeya, tare da
dukan ma'aikatansa kewaye da shi. 7 Ya ce musu, "Mutanen Benyamin, ku saurara;
ɗan Yesse zai iya ba dukanku filaye da gonakin inabi ne? Zai ba dukanku shugabanci
na dubbai ko shugabanci na ɗari-ɗari? 8 Abin da ya sa dukanku kuka gama baki a
kaina? Ba wanda ya gaya mini lokacin da ɗana ya yi yarjejjeniya da ɗan Yesse, ba
wanda ya kulla da ni, ko ya gaya mini cewa ɗana ya sa bawana yă tayar mini, yana
fakona kamar yadda yake a yau."

9 Amma Doyeg mutumin Edom da yake tsaye tare da fadawan Shawulu ya ce, "Na
ga ɗan Yesse ya zo wurin Ahimelek ɗan Ahitub a Nob. 10 Ahimelek ya roƙi UBANGIJI
saboda shi, ya kuma ba shi guzuri da takobin Goliyat Bafilistin."

11 Sai sarki ya aika aka kira masa Ahimelek firist ɗan Ahitub da dukan iyalin
mahaifinsa. Dukansu suka zo wurin sarki. 12 Shawulu ya ce, "Ka saurara yanzu,
ɗan Ahitub."

Ya amsa ya ce, "Ina saurara, ranka yă daɗe."

13 Shawulu ya ce masa, "Don me ka gama baki da ɗan Yesse a kaina har ka ba shi
burodi da takobin (Goliyat), ka kuma roƙi Allah don yă tayar mini, yă kuma yi fakona
kamar yadda yake yi yau?"

14 Ahimelek ya ce wa sarki, "A cikin bayinka duka, wa ke da aminci iri na Dawuda,
surukin sarki, shugaban jarumanka wanda ake girmamawa da gaske a gidanka? 15 A
wannan rana ce da na fara roƙon Allah saboda shi? Kada sarki yă zargi bawansa ko
wani daga iyalin mahaifinsa, gama bawanka bai san kome a kan dukan waɗannan
al'amura ba."

16 Amma sarki ya ce, "Lalle Ahimelek za ka mutu, da kai da dukan iyalin
mahaifinka."

17 Sai sarki ya umarci matsaran da suke tsaye kusa da shi ya ce, "Ku kakkashe
firistocin UBANGIJI, gama su ma sun goyi bayan Dawuda. Sun san yana gudu, duk da
haka ba su gaya mini ba."

Amma ma'aikatan sarki ba su yarda su sa hannu su kashe firistocin UBANGIJI ba.

18 Sai sarki ya umarce Doyeg ya ce, "Ka juya ka kakkashe firistocin." Doyeg
mutumin Edom ya juya ya kakkashe firistocin. A ranar kuwa ya kashe mutum
tamanin da biyar waɗanda suke sanye da efod na lilin. 19 Ya kuma hallaka Nob
birnin firistoci, ya kashe dukan mata, da maza, da yara, da jarirai, da shanu, da
jakuna, da kuma tumaki.

20 Amma Abiyatar ɗan Ahimelek jikan Ahitub ya tsere, ya gudu zuwa wurin
Dawuda. 21 Abiyatar gaya wa Dawuda cewa, "Shawulu ya hallaka firistocin UBANGIJI."
22 Dawuda ya ce wa Abiyatar, "Lalle a wancan ranar, sa'ad da na ga Doyeg mutumin
Edom a can, na san tabbatacce zai gaya wa sarki. Ni ne sanadin mutuwar dukan
iyalin mahaifinka. 23 Ka zauna tare da ni, kada ka ji tsoro mutumin da yake neman
ranka, yana nema raina ma. Ka zauna lafiya tare da ni."

# 23

### *Dawuda ya ceci Keyila*

1 Sa'ad da aka ce wa Dawuda, "Duba ga Filistiyawa suna yaƙi da mutanen Keyila,
suna kwashe musu hatsi a masussukai." 2 Sai Dawuda ya nemi nufin UBANGIJI, ya ce,
"In tafi in fāɗa wa Filistiyawa da yaƙi?"

UBANGIJI kuwa ya ce masa, "Jeka ka yi yaƙi da Filistiyawa, ka ceci Keyila."

3 Amma mutanen Dawuda suka ce masa, "Ga shi, a nan ma a Yahuda muna jin
tsoro, balle mu tafi Keyila mu yi yaƙi da sojojin Filistiyawa!"

4 Dawuda ya sāke nemi nufin UBANGIJI, sai UBANGIJI ya ce masa, "Tashi ka gangara
zuwa Keyila, gama zan ba da Filistiyawa a hannunka." 5 Sa'an nan Dawuda
da mutanensa suka tafi Keyila, suka yi yaƙi da Filistiyawa, suka kwashe musu
shanunsu, suka jijji wa Filistiyawa ƙwarai, suka cece mutanen Keyila daga hannunsu.
6 (Abiyatar ɗan Ahimelek ya zo da efod sa'ad da ya gudo zuwa wurin Dawuda a
Keyila.)

### *Shawulu ya fafari Dawuda*

7 Shawulu ya sami labari cewa Dawuda ya tafi Keyila, sai ya ce, "Allah ya bashe
shi a hannuna, domin Dawuda ya kulle kansa ke nan da ya shiga birnin da yake
da ƙofofin da ake kulle da ƙarafa." 8 Shawulu ya kira dukan sojojinsa don yaƙi, su
gangaro zuwa Keyila su mamaye Dawuda da mutanensa.

9 Da Dawuda ya ji labari Shawulu yana shirya hanyar da zai kashe shi, sai ya ce
wa Abiyatar firist, "Kawo mini efod a nan." 10 Dawuda ya ce, "Ya UBANGIJI, Allah na
Isra'ila, bawanka ya sami labari cewa tabbatacce Shawulu yana shirin zuwa Keyila
yǎ hallaka garin saboda ni. 11 Mutanen Keyila za su bashe ni a gare shi? Shawulu zai
gangaro nan kamar yadda bawanka ya sami labari? Ya UBANGIJI, Allah na Isra'ila, ka
gaya wa bawanka."

UBANGIJI ya ce, "Zai zo."

12 Dawuda ya sāke cewa, "Mutanen Keyila za su bashe ni da mutanena ga
Shawulu?"

UBANGIJI ya ce, "Za su yi."

13 Saboda haka Dawuda da mutanensa wajen mutum ɗari shida suka bar Keyila,
suka yi ta tafiya daga wannan wuri zuwa wancan. Sa'ad da aka gaya wa Shawulu
cewa Dawuda ya tsere daga Keyila, sai ya fasa tafiya can.

14 Dawuda ya zauna a jeji cikin kogunan duwatsu da kuma tuddan jejin Zif. Kowace
rana Shawulu ya yi ta neman Dawuda amma Allah bai bashe Dawuda a hannunsa
ba.
15 A lokacin da Dawuda yana zaune a Horesh cikin jejin Zif, ya sami labari cewa
Shawulu ya fito don yă kashe shi. 16 Yonatan ɗan Shawulu kuwa ya tafi wurin
Dawuda a Horesh, ya ƙarfafa shi yă dogara ga Allah. 17 Ya ce, "Kada ka ji tsoro,
mahaifina Shawulu ba zai taɓa sa hannu a kanka ba. Za ka zama sarki a Isra'ila, ni
kuma in zama na biyu gare ka. Kai, ko mahaifina Shawulu ma ya san da haka." 18 Su
biyunsu kuwa suka ɗaura yarjejjeniya a gaban Ubangiji. Sai Yonatan ya koma gida
amma Dawuda ya zauna Horesh.
19 Zifawa suka tafi wurin Shawulu a Gibeya suka ce masa, "Ashe, ba Dawuda ne
yake ɓuya a cikinmu a kogwannin duwatsu a Horesh a bisan tudun Hakila, kudu da
Yeshimon ba? 20 Yanzu, ya sarki, ka gangaro, ka zo a duk lokacin da ka ga ya yi maka,
ka zo mu kuma hakkinmu ne mu bashe shi a hannun sarki."
21 Shawulu ya ce, "Ubangiji ya yi muku albarka, gama kun damu da ni. 22 Ku tafi
ku ƙara shiri. Ku san inda yakan tafi, wane ne kuma ya gan shi a can. An gaya mini
cewa shi mai wayo ne sosai. 23 Ku binciko duk wuraren da yakan ɓuya, sai ku dawo
ku gaya mini tabbataccen labari. Sa'an nan zan tafi tare da ku in yana can. Zan nemi
shi ko'ina cikin dukan kabilar Yahuda."
24 Sai suka tashi suka koma Zif, suka sha gaban Shawulu. Dawuda da mutanensa
kuwa suna jejin Mawon cikin Araba, kudu da Yeshimon. 25 Shawulu da mutanensa
suka tafi neman Dawuda. Da Dawuda ya ji labari, sai ya gangara cikin duwatsu ya
zauna a cikin jejin Mawon. Sa'ad da Shawulu ya ji haka, sai ya tafi jejin Mawon yana
fafaran Dawuda.
26 Shawulu yana tafiya a gefe ɗaya na dutsen, Dawuda da mutanensa kuma suna
a wancan gefe, suna hanzari su ɓace wa Shawulu. Sa'ad da Shawulu da sojojinsa
suka kusa cimma Dawuda da mutanensa don su kama su, 27 sai wani manzo ya zo
wurin Shawulu yana cewa, "Ka koma da sauri, Filistiyawa sun kawo wa ƙasar hari."
28 Shawulu kuwa ya janye daga fafaran Dawuda, ya tafi yă ƙara da Filistiyawa. Dalilin
ke nan da ake kiran wannan wuri Sela Hammalekot, wato, dutsen tserewa. 29 Dawuda
kuwa ya haura daga can ya zauna a kogwannin duwatsun En Gedi.

# 24

*Dawuda ya bar Shawulu da rai*

1 Bayan da Shawulu ya komo daga fafaran Filistiyawa, sai aka gaya masa cewa,
"Dawuda yana can a Jejin En Gedi." 2 Saboda haka Shawulu ya zaɓi mutum dubu uku
daga cikin dukan Isra'ila, suka fita neman Dawuda da mutanensa kusa da Duwatsun
Awakin Jeji.
3 Da Shawulu ya isa inda ake ajiye garken tumaki a bakin hanya inda akwai kogo,
sai ya shiga ciki kogon don yă yi bayan gari. Dawuda da mutanensa kuwa suna can
zaune a ƙurewar kogon. 4 Mutanen Dawuda suka ce, wannan rana ce Ubangiji ya yi
magana ya ce maka, "Zan ba da maƙiyinka a hannunka domin ka yi abin da ka ga
dama da shi." Sai Dawuda ya tashi a hankali ya je ya yanke shafin rigar Shawulu.
5 Daga baya Dawuda ya damu domin ya yanke shafin rigar Shawulu. 6 Ya ce wa
mutanensa, "Ubangiji yă sawwaƙe in yi abu haka ga shugabana da Ubangiji ya shafe,
ko in ɗaga hannuna in kashe shi, gama shi shafaffe ne na Ubangiji." 7 Da wannan
magana Dawuda ya kwaɓi mutanensa, bai yarda su fāɗa wa Shawulu ba. Shawulu
kuwa ya bar kogon ya yi tafiyarsa.
8 Daga baya Dawuda ya fita daga kogon sai ya kira Shawulu ya ce, "Ranka yă daɗe,
sarki!" Da Shawulu ya waiwaya, sai Dawuda ya rusuna da fuskarsa har ƙasa. 9 Ya

ce wa Shawulu, “Me ya sa kake saurari mutanen da suke cewa, ‘Dawuda ya dāge
yă cuce ka’? 10 Yau ka ga da idonka yadda UBANGIJI ya bashe ka a hannuna a cikin
kogon nan. Waɗansu sun ce mini in kashe ka, amma na bar ka, na ce, ‘Ba zan sa
hannuna a kan shugabana ba, gama shi shafaffe ne na UBANGIJI.’ 11 Babana, duba, ga
shafin rigarka a hannuna, na yanke shafin rigarka amma ban kashe ka ba. Yanzu ka
gane ka kuma sani cewa ba ni da laifin aikata kome ko tayarwa, ban yi maka laifi ba,
amma kana farautar raina. 12 UBANGIJI zai shari’anta tsakanina da kai. UBANGIJI zai
sāka mini laifin da ka yi mini, amma ni kam ba zan taɓa ka ba. 13 Kamar yadda karin
maganan nan na dā ya ce, ‘Daga cikin masu mugunta, mugunta ke fitowa,’ hannuna
dai ba zai taɓa ka ba.
14 “Wane ne sarkin Isra’ila, ka fito kake bi? Wa kake kora? Kana bin mataccen
kare ko kuɗin cizo? 15 UBANGIJI yă zama alƙali, yă yi shari’a tsakanina da kai, bari
UBANGIJI yă duba, yă tsaya mini, yă nuna ba ni da laifi.”
16 Da Dawuda ya gama wannan magana, sai Shawulu ya ce, “Muryarka ke nan ɗana
Dawuda?” Sai ya fasa da kuka. 17 Ya ce, “Ka fi ni gaskiya, ka yi mini alheri, ni kuwa
na yi maka mugunta. 18 Ga shi yanzu ka faɗa mini alherin da ka yi mini. UBANGIJI ya
bashe ni a hannunka amma ba ka kashe ni ba. 19 In mutum ya sami maƙiyinsa, zai
bar shi yă tafi lafiya ba tare da yin masa rauni ba? UBANGIJI yă sāka maka, gama ka
nuna mini alheri a yau. 20 Na sani tabbatacce za ka zama sarki. Masarautar Isra’ila
za tă kahu a hannunka. 21 Yanzu ka rantse mini da UBANGIJI cewa ba za ka hallaka
zuriyarta ko ka share sunana daga iyalin mahaifina ba.”
22 Sai Dawuda ya rantse wa Shawulu. Sa’an nan Shawulu ya koma gida, amma
Dawuda da mutanensa suka haura zuwa wurin ɓuya.

# 25

*Dawuda da Nabal da Abigiyel*

1 Sama’ila ya rasu, sai dukan Isra’ila suka taru suka yi makoki saboda shi. Suka
binne shi a gidansa a Rama. Sai Dawuda ya gangara zuwa cikin Jejin Faran.
2 A Mawon, akwai wani mutum wanda yake da dukiya a Karmel, mutumin mai
arziki ne ƙwarai. Yana da awaki dubu ɗaya, da tumaki dubu uku waɗanda yake wa
aski a Karmel. 3 Ana ce da shi Nabal, sunan matarsa kuwa Abigiyel. Tana da hikima
ga ta kuma kyakkyawa, amma mijinta mai rowa ne marar mutunci. Shi daga kabilar
Kaleb ne.
4 Lokacin da Dawuda yake a jeji, ya ji labari cewa Nabal yana askin tumaki. 5 Sai
ya zaɓi samari goma ya aike su wurin Nabal a Karmel su gaishe shi a madadinsa,
6 su ce masa, “Ranka yă daɗe, ina maka fatan alheri, kai da gidanka da dukan abin
da kake da shi!
7 “Na ji cewa, yanzu lokacin askin tumaki ne. Sa’ad da makiyayanka suke tare da
mu, ba mu cuce su ba, kuma duk zamansu a Karmel ba abin da yake nasu da ya ɓata.
8 Ka tambayi bayinka za su kuwa gaya maka. Saboda haka ka yi wa mutanena kirki,
gama yau ranar biki ce. Ina roƙonka ka ba wa samarina, wato, bayinka, da ni ɗanka
Dawuda, duk abin da kake iya ba su.”
9 Da mutanen Dawuda suka isa wurin Nabal, suka ba wa Nabal wannan saƙo a
sunan Dawuda, sai suka jira.
10 Nabal ya ce wa mutanen Dawuda, “Wane ne wannan Dawuda? Wane ne wannan
ɗan Yesse? Yawancin bayi suna tayar wa iyayengijinsu a kwanakin nan. 11 Don me
zan ɗauki burodina da ruwana, da kuma naman da na yanka saboda masu yin wa
tumakina aski in ba mutanen da ban ma san inda suka fito ba?”
12 Mutanen Dawuda suka juya suka koma. Da suka iso sai suka faɗa wa Dawuda
abin da Nabal ya ce. 13 Dawuda ya ce wa mutanensa, “Kowa yă rataya takobinsa.”

Sai duk suka yi haka. Dawuda kuma ya rataya nasa. Mutum wajen ɗari huɗu suka tafi tare da Dawuda, mutum ɗari biyu kuwa suka zauna suna gadin kayansu.

14 Ɗaya daga cikin bayin Nabal ya gaya wa Abigiyel matar Nabal cewa, "Dawuda ya aiko da bayinsa daga jeji su gai da maigida, amma maigida ya zazzage su.
15 Waɗannan mutane kuwa sun yi mana kirki ƙwarai, ba su ba mu wata wahala ba. Babu abu guda da ya ɓace mana dukan lokacin da muke tare da su. 16 Dare da rana sun zama mana katanga kewaya da mu, a duk tsawon lokacin da muke kiwon tumakinmu kusa da su. 17 Ki yi nazari a kai, ki ga ko za ki iya yin wani abu, domin masifa yana nan rataye a wuyan maigidanmu da dukan iyalin gidansa. Shi mugun mutum ne wanda ba wani da zai iya yin masa magana."

18 Abigiyel ba tă ɓata lokaci ba. Ta ɗauki burodi guda ɗari biyu, da salkar ruwan inabi biyu da tumaki biyar da aka gyara, da soyayyen hatsi mudu biyar, da waina guda ɗari na 'ya'yan inabi, da masa ɗari biyu na kauɗar ɓaure ta labta wa jakuna.
19 Sai ta ce wa bawanta, "Yi gaba, zan bi ka". Amma ba tă gaya wa Nabal, mijinta ba.

20 Da tana tafiya a kan jaki, ta kai gindin wani dutse ke nan, sai ga Dawuda da mutanensa suna gangarowa zuwa wajen da take. Sai ta tafi, ta sadu da su. 21 Bai daɗe ba da Dawuda ya ce a ransa, "Ashe, a banza ne na yi ta lura da dukan abin da yake na mutumin nan a jeji, har ba abinsa da ya ɓace. Ga shi, ya rama mini alheri da mugunta. 22 Bari Allah yă yi duk abin da ya ga dama da ni in na bar ko ɗaya daga mazan da suke da tare shi, gobe da safe."

23 Da Abigiyel ta ga Dawuda, sai ta gaggauta ta sauka daga kan jaki, ta rusuna a gaban Dawuda da fuskarta har ƙasa. 24 Ta fāɗi a ƙafafunsa ta ce, "Bari laifin yă zama nawa, ranka yă daɗe. Ina roƙonka ka bar baiwarka ta yi magana, ka ji abin da baiwarka za tă ce. 25 Kada ranka yă daɗe, yă kula da Nabal, mugun mutumin nan. Shi dai kamar sunansa ne, sunansa Wawa ne, kuma wawanci yana cikinsa. Amma ni baiwarka, ban ga mutanen da ranka yă daɗe ya aika ba. 26 Da yake yanzu, ya mai girma, UBANGIJI ya hana ka zubar da jini da kuma ɗaukan wa kanka fansa, muddin UBANGIJI yana raye, kai kuma kana a raye, bari maƙiyinka da dukan waɗanda suke niyya su cuci shugabana su zama kamar Nabal. 27 Bari kuma ka karɓi wannan kyautar da baiwarka ta kawo don samarin da suke binka. 28 Ina roƙonka ka gafarta wa baiwarka laifinta gama tabbatacce UBANGIJI zai ba shugabana dawwammamiyar sarauta, gama kana yin yaƙin UBANGIJI ne. Kuma ba wani mugun abin da zai same ka muddin kana a raye. 29 Ko da yake wani mutum yana fafaranka domin yă kashe ka, UBANGIJI Allahnka zai kiyaye ranka. Amma za a wurgar da rayukan maƙiyanka kamar yadda ake wurga dutsen majajjawa. 30 Sa'ad da UBANGIJI ya cika kowane alherinsa da ya yi wa shugabana alkawari, ya kuma keɓe shi sarki a bisa Isra'ila,
31 kada yă zama cewa zuciyarka ta ba ka laifi ko ka damu cewa kana da alhakin jini, kada ka yi ramuwa da kanka. Sa'ad da UBANGIJI ya nuna maka alheri, ka tuna da ni, baiwarka."

32 Dawuda ya ce wa Abigiyel, "Yabo ya tabbata ga UBANGIJI, Allah na Isra'ila, wanda ya aiko ki don ki same ni yau. 33 Bari Allah yă albarkace ki saboda hikima yanke hukuncinki da kuma hana ni zubar da jini da ɗauka wa kaina fansa da hannuna a wannan rana. 34 UBANGIJI, ya hana ni in yi miki ɓarna. Da ba don kin zo kin sadu da ni ba, na rantse da UBANGIJI, Allah na Isra'ila Mai Rai, babu ko ɗaya daga cikin mazan gidan Nabal da zai rage gobe da safe."

35 Sa'an nan Dawuda ya karɓi abin da ta kawo masa daga hannunta, ya kuma ce mata, "Ki koma gida kada ki damu, na ji koke-kokenki, zan kuma biya miki bukatarki."

36 Da Abigiyel ta kai gida sai ta sami Nabal cikin gida yana ta fama biki iri na sarakuna. Yana ji wa ransa daɗi, ya kuma bugu tilis, saboda haka ba tă ce masa

kome ba sai da gari ya waye. 37 Da safe sa'ad da Nabal ya natsu, sai matarsa ta gaya
masa dukan abin da ya faru. Sai zuciyarsa ta tsinke, ya zama kamar dutse. 38 Bayan
kusan kwana goma, Ubangiji ya bugi Nabal, sai ya mutu.
39 Da Dawuda ya sami labarin mutuwar Nabal, sai ya ce, "Yabo ya tabbata ga
Ubangiji, wanda ya sāka mini a kan irin renin da Nabal ya yi mini. Ya hana bawansa
yin mugunta, ga shi ya ɗora wa Nabal muguntar da ya yi."
Sai Dawuda ya aika wa Abigiyel cewa tă zama matarsa. 40 Bayin Dawuda suka tafi
Karmel suka ce wa Abigiyel, "Dawuda ya aike mu gare ki, mu zo mu ɗauke ki ki zama
matarsa."
41 Sai ta rusuna da fuskarta har ƙasa ta ce, "Ni baranyarka ce, na shirya in bauta
maka in kuma wanke ƙafafun bayin shugabana." 42 Abigiyel ta tashi da sauri ta hau
jaki, ta kuma sa 'yan mata biyar da suke mata hidima su bi ta, suka tafi tare da
'yan saƙon Dawuda. Ta kuwa zama matarsa. 43 Dawuda a lokacin ya riga ya auri
Ahinowam daga Yezireyel, dukansu suka zama matansa. 44 Amma Shawulu ya aurar
da Mikal, 'yarsa, matar Dawuda, ga Falti ɗan Layish wanda yake daga Gallim.

# 26

*Dawuda ya sāke barin Shawulu da rai*

1 Zifawa suka je wurin Shawulu a Gibeya suka ce, "Ashe, ba Dawuda ne ya ɓuya a
tudun Hakila da yake fuskantar Yeshimon ba?"
2 Sai Shawulu ya tashi ya gangara zuwa Jejin Zif, tare da zaɓaɓɓun mutane dubu
uku na Isra'ila. Suka fita neman Dawuda a can. 3 Shawulu ya yi sansani a bakin
hanyar zuwa tudun Hakila mai fuskantar Yeshimon. Amma Dawuda yana zaune a
jeji. Sa'ad da ya ga Shawulu ya biyo shi har zuwa can, 4 sai ya aiki 'yan leƙen asiri
su tabbata lalle Shawulu ya iso can.
5 Sai Dawuda ya kintsa ya tafi inda Shawulu ya yi sansani. Ya ga inda Shawulu da
Abner ɗan Ner shugaban ƙungiyar soja suka kwanta. Shawulu yana kwance a cikin
sansani tare da sojoji kewaye da shi.
6 Sai Dawuda ya ce wa Ahimelek mutumin Hitti da Abishai ɗan Zeruhiya ɗan'uwan
Yowab, "Wa zai gangara tare da ni zuwa sansanin Shawulu?"
Sai Abishai ya ce, "Zan tafi tare da kai."
7 Saboda haka Dawuda da Abishai suka gangara zuwa wurin rundunar da dare, sai
ga Shawulu kwance yana barci a cikin sansani da māshinsa a kafe a ƙasa kusa da
kansa. Abner kuwa tare da sojoji suna kwance kewaye da shi.
8 Abishai ya ce wa Dawuda, "Yau Allah ya ba da maƙiyinka a hannunka. Bari in
kafe shi da ƙasa da māshina, zan soke shi da māshi sau ɗaya tak, ba na bukata in
soke shi sau biyu."
9 Amma Dawuda ya ce wa Abishai, "Kada ka hallaka shi. Wa zai sa hannu a kan
shafaffe na Ubangiji, har yă tsira? 10 Muddin Ubangiji yana a raye, Ubangiji da kansa
zai buge shi, ko yă mutu a lokacinsa, ko kuma yă mutu a wurin yaƙi. 11 Amma Allah
yă sawwaƙa in sa hannu a shafaffen Ubangiji, ka ɗauki māshin da butar ruwan da
take kusa da kansa mu tafi."
12 Saboda haka Dawuda ya ɗauki māshin da butar ruwan da take kusa da Shawulu
suka tafi. Ba wanda ya gan su, ba wanda ya san abin da ya faru, ba kuwa wanda ya
farka, dukansu suna barci gama Ubangiji ya sa barci mai nauyi ya ɗauke su.
13 Sa'an nan Dawuda ya haye zuwa wancan gefen kwarin, ya hau kan wani tudu
mai ɗan nisa inda Shawulu tare da mutanensa suke. Akwai babban fili tsakaninsu.
14 Sai Dawuda ya kira sojojin Shawulu da kuma Abner ɗan Ner ya ce, "Abner ba za
ka amsa mini ba?"
Abner ya ce, "Wane ne yake kira yana damun sarki haka?"

15 Dawuda ya ce wa Abner, "Wane irin mutum ne kai? Ba kai ne soja mafi iya yaƙi
a Isra'ila ba? Don me ba ka yi gadin ranka yă daɗe, sarki da kyau ba? Ɗazu wani ya
shiga tsakiyarku don yă kashe ranka yă daɗe, sarki. 16 Abin da ka yi bai yi kyau ba.
Muddin UBANGIJI yana a raye kai da mutanenka kun cancanci mutuwa, domin ba ku
lura da maigidanku shafaffe na UBANGIJI ba. Ka duba kewaye da kai, ina māshi da
kuma butar ruwan da suke kusa da kansa?"
17 Shawulu ya gane muryar Dawuda, sai ya ce, "Muryarka ke nan ɗana Dawuda?"
Dawuda ya ce, "I, muryata ce ya ranka yă daɗe, sarki." 18 Ya ƙara da cewa, "Don
me ranka yă daɗe, yake fafarata? Mene ne na yi? Wane abu ne aka same ni da laifi
a kai? 19 To, bari ranka yă daɗe, sarkina yă kasa kunne yă ji abin da zan faɗa. Idan
UBANGIJI ne ya sa ka yi fushi da ni, bari yă karɓi hadaya ta hatsi. Amma idan mutane
ne suka sa ka, bari a la'anta su, UBANGIJI ne shaidata. Gama sun kore ni don kada
in sami rabo cikin gādon UBANGIJI, suna cewa, 'Ka je ka bauta wa waɗansu alloli.'
20 Kada ka yarda jinina yă zuba a ƙasa nesa da gaban UBANGIJI. Sarkin Isra'ila ya fito
yă nemi kuɗin cizo kamar mai farautar kazan duwatsu."
21 Sai Shawulu ya ce, "Na yi zunubi ka dawo Dawuda ɗana. Ba zan yi maka kome
ba, domin ka darajarta raina yau. Lalle na yi wawanci! Na yi babban kuskure."
22 Dawuda ya ce, "Ga māshin sarki, ka aiko wani saurayi yă zo yă karɓa. 23 UBANGIJI
yakan sāka wa kowa bisa ga adalcinsa da amincinsa. UBANGIJI ya bashe ka a hannuna
yau, amma ba zan sa hannuna a kan shafaffe na UBANGIJI ba. 24 Kamar yadda na ga
darajar ranka yau. Haka ma bari UBANGIJI yă ga darajar raina, yă cece ni daga dukan
wahala."
25 Sai Shawulu ya ce wa Dawuda, "Allah yă albarkace ka ɗana, Dawuda, za ka yi
manyan abubuwa, tabbatacce kuma ka yi nasara."
Sai Dawuda ya yi tafiyarsa, Shawulu kuwa ya koma gida.

# 27

*Dawuda a cikin Filistiyawa*

1 Dawuda ya yi tunani a ransa ya ce, "Wata rana Shawulu zai kashe ni, abu mafi
kyau da zan yi shi ne in tsere zuwa ƙasar Filistiyawa. Da haka Shawulu zai fid da
zuciya ga nemana a ƙasar Isra'ila, a can kuwa zan tsira daga hannunsa."
2 Sai Dawuda tare da mutanensa, mutum ɗari shida suka tashi suka haye zuwa
wurin Akish ɗan Mawok, sarkin Gat. 3 Dawuda da mutanensa suka zauna a Gat tare
da Akish. Kowa ya kasance tare da iyalinsa. Dawuda kuwa yana tare da matansa
biyu. Ahinowam daga Yezireyel da Abigiyel matar Nabal da ya mutu daga Karmel.
4 Da Shawulu ya sami labari cewa Dawuda ya gudu zuwa Gat, bai ƙara fita nemansa
ba.
5 Sai Dawuda ya ce wa Akish, "In na sami tagomashi a gabanka ka ba ni wani wuri
a cikin biranenka in zauna a can. Don me bawanka zai kasance tare da kai a gidan
sarauta?"
6 A ranar Akish ya ba shi Ziklag wanda tun dā take ta sarkin Yahuda. 7 Dawuda ya
zauna a yankin Filistiyawa shekara ɗaya da wata huɗu.
8 Dawuda da mutanensa suka haura suka yaƙi Geshurawa, da Girziyawa, da
Amalekawa. (Waɗannan su ne mazaunan ƙasar a dā, tun daga Shur har zuwa ƙasar
Masar.) 9 Duk lokacin da ya yaƙi wani wuri, ba ya barin namiji ko mace da rai, amma
sai ya kwashe tumaki, da shanu, da jakuna, da raƙuma, da riguna, sa'an nan yă koma
wurin Akish.
10 Idan Akish ya ce, "Ina ka kai hari yau?" Sai Dawuda yă ce, "Na kai hari a Negeb
ta Yahuda, ko Negeb ta Yerameyel, ko Negeb na Keniyawa." 11 Bai bar a kawo namiji
ko mace da rai a Gat ba, gama yana tunani, "Za su ba da sanarwa a kanmu su ce,
'Ga abin da Dawuda ya yi.' " Haka ya yi ta yi dukan rayuwarsa a ƙasar Filistiyawa.

12 Akish ya amince da Dawuda sosai, har ya ce wa kansa, “Ga shi ya mai da kansa
abin ƙi ga mutanensa Isra’ilawa, zai zama bawana har abada.”

# 28

1 Filistiyawa suka tattara sojojinsu domin su yaƙi Isra’ila. Akish ya ce wa Dawuda,
“Sai ka sani fa, kai da mutanenka za ku tafi tare da ni da sojojina.”

2 Dawuda ya ce, “Kai da kanka za ka ga abin da bawanka zai yi.”

Akish ya ce, “Da kyau, zan sa ka zama mai kāre ni.”

### *Shawulu da Maiyar En Dor*

3 Sama’ila dai ya riga ya rasu, dukan Isra’ila suka yi makokinsa suka binne shi a
garinsa a Rama. Shawulu kuma ya kori duk masu duba da masu maitanci daga ƙasar.

4 Filistiyawa suka tattaru suka yi sansani a Shunem. Shawulu ya tattara dukan
Isra’ila suka yi sansani a Gilbowa. 5 Da Shawulu ya ga sojojin Filistiyawa sai ya ji
tsoro, ya firgita ƙwarai. 6 Ya nemi nufin Ubangiji amma bai sami amsa daga wurin
Ubangiji ko ta wurin mafarki, ko ta wurin Urim, ko ta wurin annabawa ba. 7 Shawulu
ya ce wa fadawansa, “Ku nemo mini wata mace mai duba domin in tafi wurinta in
yi tambaya.”

Suka ce, “Akwai guda a En Dor.”

8 Sai Shawulu ya sa waɗansu tufafi ya ɓad da kama, shi da waɗansu mutum biyu
suka tafi wurin matar da dare, ya ce mata, “Ki yi mini duba ta hanyar sihiri, ki hawar
mini duk wanda zan faɗa miki.”

9 Amma matar ta ce masa, “Tabbatacce ka dai san abin da Shawulu ya yi, ya
karkashe masu duba da masu maitanci a ƙasar. Me ya sa kake sa mini tarko, don ka
sa a kashe ni?”

10 Shawulu ya rantse mata da Ubangiji. Ya ce, “Muddin Ubangiji yana a raye, ba za
a hukunta ki a kan wannan ba.”

11 Sai matar ta ce, “Wa kake so in hauro maka?”

Sai ya ce, “Ki hauro mini da Sama’ila.”

12 Da matar ta ga Sama’ila sai ta yi ihu da ƙarfi ta ce wa Shawulu, “Me ya sa ka
ruɗe ni? Kai ne Shawulu!”

13 Sai sarki ya ce mata, “Kada ki ji tsoro. Me kika gani?”

Matar ta ce, “Na ga wani kurwa tana fitowa daga ƙasa.”

14 Ya ce, “Yaya kamanninsa yake?”

Ta ce, “Wani tsoho sanye da taguwa ne yake haurawa.”

Shawulu ya gane cewa Sama’ila ne, sai ya rusuna da fuskarsa har ƙasa.

15 Sama’ila ya ce wa Shawulu, “Don me ka dame ni, ta wurin hauro da ni?”

Shawulu ya ce, “Ina cikin babban damuwa ce, Filistiyawa sun fāɗa mini, Allah
kuma ya juya mini baya. Bai amsa mini, ko ta mafarki, ko kuma ta annabawa ba,
saboda haka na kira ka don ka gaya mini abin yi.”

16 Sama’ila ya ce, “Don me kake tambayata bayan Ubangiji ya rabu da kai? Ya
zama maƙiyinka? 17 Ubangiji ya cika abin da ya yi magana ta wurina. Ubangiji ya
fizge mulki daga hannunka, ya ba maƙwabcinka Dawuda. 18 Gama ba ka yi biyayya
ga Ubangiji ba, ba ka zartar da hukuncinsa mai zafi a kan Amalekawa ba. Saboda
haka Ubangiji ya yi maka haka yau. 19 Ubangiji zai ba da Isra’ila da kuma kai ga
Filistiyawa, gobe kuwa da kai da ’ya’yanka za ku kasance tare da ni. Ubangiji kuma
zai ba da sojojin Isra’ila a hannun Filistiyawa.”

20 Da jin maganar Sama’ila sai Shawulu ya faɗi ƙasa warwas. Tsoro ya kama shi
ƙwarai. Ba shi kuma da ƙarfi domin bai ci kome ba dukan yini da kuma dukan dare.

21 Da matar ta zo wurin Shawulu, ta ga shi a firgice, sai ta ce masa, "Duba
baranyarka ta yi maka biyayya ta yi kasai da ranta, ta yi abin da ka ce ta yi. 22 To, kai
ma ka kasa kunne ga baranyarka, zan ba ka abinci ka ci don ka sami ƙarfin tafiya."
23 Sai ya ƙi. Ya ce, "Ba zan ci abinci ba."

Sai da bayinsa da matar suka roƙe shi, sa'an nan ya ji maganarsu, ya tashi daga ƙasa, ya zauna a bakin gado.

24 Matar kuwa tana da maraƙin da take kiwo a gida, sai ta ɗauke shi nan da nan
ta yanka. Ta ɗauki garin fulawa ta kwaɓa, ta yi waina marar yisti. 25 Sai ta kawo wa
Shawulu da bayinsa suka kuwa ci. A daren nan suka tashi suka tafi.

# 29

## *Akish ya mai da Dawuda Ziklag*

1 Filistiyawa suka tattara dukan rundunoninsu a Afek. Isra'ila kuwa suka yi sansani
kusa da maɓulɓular da take Yezireyel. 2 Sa'ad da sarakuna Filistiyawa suke wucewa
da rundunarsu na mutum ɗari-ɗari da na dubu-dubu. Dawuda da mutanensa suna
biye a baya tare da Akish. 3 Komandodin Filistiyawa suka ce, "Waɗannan Ibraniyawa
kuma fa?"

Akish ya ce, "Wannan shi ne Dawuda hafsan Shawulu, sarkin Isra'ila. Yana nan tare da ni shekara guda ke nan. Ban kuwa taɓa samunsa da wani lahani ba tun daga ranar da ya bar Shawulu."

4 Amma komandodin Filistiyawa suka yi fushi, suka ce, "Ka sa mutumin nan yǎ
koma zuwa wurin da ka ba shi yǎ zauna. Ba zai bi mu zuwa wurin yaƙi ba. Yana
iya juya a kanmu lokacin yaƙin. Zai iya yin amfani da wannan zarafi yǎ ciccire
kawunanmu don yǎ faranta wa maigidansa rai? 5 Tuna fa, ba shi ne Dawuda ɗin da
ake girmama da rawa da waƙoƙi ana cewa,

" 'Shawulu ya kashe dubbai,
Dawuda kuwa dubbun dubbai ba'?"

6 Saboda haka Akish ya kira Dawuda ya ce masa, "Muddin UBANGIJI yana a raye,
na amince da kai tun daga ranar da ka zo wurina har yǎ zuwa yau, ban same ka
da wani laifi ba, na kuma yi farin ciki in sa ka a cikin sojojina don ka yi mini aiki.
Amma masu mulki nawa ba su yarda da kai ba. 7 Sai ka juya ka koma ka isa lafiya
ba tare da ɓata wa masu mulkin Filistiyawa rai ba."

8 Dawuda ya ce wa Akish, "Me na yi? Ka taɓa samun bawanka da laifi tun daga
ranar da na zo har zuwa yanzu? Ina dalilin da ba zan tafi tare da kai in yaƙi maƙiyin
ranka yǎ daɗe, sarki ba?"

9 Akish ya ce, "A ganina kai marar laifi ne kamar mala'ikan Allah, duk da haka
shugabannin sojojin Filistiyawa sun ce, 'Ba zai tafi yaƙi tare da mu ba.' 10 Ka tashi
da sassafe, kai da bayin shugabanka da suka zo tare da kai. Da gari ya waye sai ku
kama hanya."

11 Gari na wayewa tun da sassafe Dawuda da mutanensa suka tashi suka kama
hanyar komawa ƙasar Filistiyawa. Filistiyawa kuwa suka haura zuwa Yezireyel.

# 30

## *Dawuda ya hallaka Amalekawa*

1 A rana ta uku, Dawuda da mutanensa suka isa Ziklag, sai suka tarar Amalekawa
sun riga sun kawo wa Negeb da Ziklag hari. Suka cinye Ziklag, suka ƙone ta, 2 suka
kwashe mata, yara da tsofaffi da dukan abubuwan da suke cikin garin. Ba su kashe
kowa ba, amma suka kwashe su, suka tafi.

3 Da Dawuda da mutanensa suka isa Ziklag suka tarar an ƙone garin, an kuma
kwashe matansu, da 'ya'yansu mata, da kuma 'ya'yansu maza ganima, 4 sai Dawuda

da mutanensa suka yi kuka, suka yi ta kuka har sai da ƙarfinsu ya ƙare. 5 An kama
matan Dawuda, wato, Ahinowam daga Yezireyel da Abigiyel matar Nabal mutumin
Karmel wanda ya rasu. 6 Dawuda kuwa ya damu ƙwarai domin mutanensa suna
niyyar su jajjefe shi da duwatsu, kowannensu ransa ya ɓace saboda 'ya'yansa maza
da mata, amma Dawuda ya sami ƙarfafawa a cikin UBANGIJI Allahnsa.

7 Sai Dawuda ya ce wa Abiyatar firist, ɗan Ahimelek, "Kawo mini efod." Sai
Abiyatar ya kawo masa. 8 Dawuda kuwa ya nemi nufin UBANGIJI ya ce, "In bi bayan
'yan harin nan? Zan ci musu?"

UBANGIJI ya ce, "Bi su, gama za ka ci musu, ka ƙwato abin da suka kwashe."

9 Dawuda da mutanensa ɗari shida suka kama hanya, da suka kai Kwarin Besor,
waɗansunsu suka tsaya a can. 10 Dawuda ya ci gaba da mutane ɗari huɗu, don
mutane ɗari biyu sun gaji sosai har sun kāsa ƙetare rafin Besor.

11 Suka sami wani mutumin Masar a fili suka kawo shi wurin Dawuda. Suka ba
shi abinci ya ci, suka kuma ba shi ruwa ya sha. 12 Suka ba shi saura wainan 'ya'yan
ɓaure da kuma wainan 'ya'yan inabi, ya ci ya sami ƙarfi. Gama bai ci ba, bai sha ba,
har yini uku da dare uku.

13 Dawuda ya tambaye shi ya ce, "Wane ne ubangidanka, kuma daga ina ka fito?"

Ya ce, "Ni mutumin Masar ne, bawan wani mutumin Amalek. Maigidana ya ƙyale
ni sa'ad da na yi rashin lafiya kwanaki ukun da suka wuce. 14 Mun kai hari a Negeb
ta Keretawa ta Yahuda, da Negeb ta Kaleb, muka kuma ƙone Ziklag."

15 Dawuda ya ce masa, "Za ka iya kai ni wurin maharan nan?"

Ya ce, "Idan ka rantse mini da Allah, ba za ka kashe ni ba, ba kuwa za ka mai da
ni wurin ubangidana ba, sai in kai ka inda maharan suke."

16 Ya bi da Dawuda har zuwa can, sai ga su a baje ko'ina a ƙasa, suna ci, suna sha,
suna annashuwa saboda yawan ganimar da suka kwashe daga ƙasar Filistiyawa da
ƙasar Yahuda. 17 Dawuda ya yaƙe su tun daga fāɗuwar rana har yammar kashegari.
Ba ko ɗaya da ya tsira sai samari ɗari huɗu waɗanda suka tsere a kan raƙuma.
18 Dawuda ya ƙwato kome da Amalekawa suka kwashe tare da matarsa biyu. 19 Babu
abin da ya ɓace, Dawuda ya dawo da kowa, manya da ƙanana, 'yan maza da 'yan
mata duka, da dukan abubuwan da Amalekawa suka kwashe. 20 Ya kuma ƙwato
garkunan tumaki, da na awaki, da na shanu. Mutanensa suka koro shanun, suka yi
gaba, suka ce, "Wannan shi ne ganimar Dawuda."

21 Da Dawuda ya zo wurin mutum ɗari biyu ɗin nan waɗanda suka tafke, suka kāsa
binsa, waɗanda aka bari a bakin Kwarin Besor, sai suka taryi Dawuda da mutanensa
da suka tafi tare da shi. Sa'ad da Dawuda ya zo kusa da su, sai ya gaishe su. 22 Sai
dukan mugaye da marasa kirki daga cikin mutanen da suka tafi tare da Dawuda suka
ce, "Tun da yake ba su tafi tare da mu ba, ba za mu ba su kome daga cikin ganimar
da muka ƙwato ba, sai dai kowane mutum yă ɗauki matarsa da 'ya'yansa yă tafi."

23 Dawuda ya ce, "A'a, 'yan'uwana ba za ku yi haka da abin da UBANGIJI ya ba
mu ba. Ya tsare mu, ya kuma bashe sojojin da suka yi gāba da mu a hannuwanmu.
24 Wa zai goyi bayanku a kan wannan al'amari? Wanda ya tafi wurin yaƙi da wanda
ya zauna wurin kaya, rabonsu zai zama daidai." 25 Dawuda ya sa wannan tă zama
dawwammamiyar farilla ga Isra'ila tun daga wannan rana har yă zuwa yau.

26 Da Dawuda ya iso Ziklag, sai ya aika wa abokansa, dattawan Yahuda da rabo daga
cikin ganimar ya ce, "Ga kyauta dominku, daga cikin ganimar maƙiyan UBANGIJI."

27 Kyautar domin waɗanda suke a Betel, da Ramot ta Negeb, da Yattir, 28 da Arower,
da Sifmot, da Eshtemowa, 29 da Rakal, da garuruwan Yerameyelawa, da garuruwan
Keniyawa, 30 da Horma, da Bor-Ashan, da Atak, 31 da Hebron, da dukan wuraren da
Dawuda da mutanensa suka taɓa zagawa.

# 31

*Shawulu ya kashe kansa*

1 Filistiyawa suka yi yaƙi da Isra'ilawa, sai Isra'ilawa suka gudu a gaban Filistiyawa,
aka kuma karkashe da yawa a dutsen Gilbowa. 2 Filistiyawa suka abka wa Shawulu
da 'ya'yansa maza, suka kashe 'ya'yan Shawulu. Yonatan da Abinadab da Malki-
Shuwa. 3 Yaƙin ya yi zafi ƙwarai kewaye da Shawulu, har maharba suka ji masa
ciwo sosai bayan sun sha ƙarfinsa.
4 Sai Shawulu ya ce wa mai ɗauka masa makami, "Ka zare takobinka ka soke ni,
kada waɗannan marasa kaciya su zo su ci mini mutunci, su kashe ni."

Amma mai ɗaukan makaman bai yarda ba don ya ji tsoro sosai. Sai Shawulu ya
zāre takobinsa ya soki kansa. 5 Da mai ɗaukar makamai ya ga Shawulu ya mutu, sai
shi ma ya zāre takobinsa ya soki kansa ya mutu. 6 Shawulu da yaransa uku da mai
ɗaukar makamansa da dukan mutanensa suka mutu a rana ɗaya.
7 Sa'ad da Isra'ilawa na bakin kwari da waɗanda suke hayin Urdun suka ga sojojin
Isra'ila suna gudu, Shawulu da yaransa uku kuma duk sun mutu, sai suka bar
mallakansu suka sheƙa da gudu. Filistiyawa kuwa suka zo suka mamaye wuraren.
8 Kashegari, da Filistiyawa suka zo domin su washe kayan matattun, sai suka tarar
Shawulu da 'ya'yansa uku duk sun mutu, a dutsen Gilbowa. 9 Suka sare kansa suka
tuɓe makamansa, suka aika manzanni a dukan ƙasar Filistiyawa, su ba da labarin
a haikalin allolinsu da cikin mutanensu. 10 Suka ajiye makaman Shawulu a cikin
haikalin gumakan Ashtarot. Suka kafa gawarsa a kan katanga Bet-Shan.
11 Sa'ad da mutanen Yabesh Gileyad suka sami labarin abin da Filistiyawa suka
yi wa Shawulu. 12 Sai dukan jarumawansu suka tashi cikin dare suka tafi Bet-Shan
suka saukar da gawar Shawulu da na 'ya'yansa daga kan katangan Bet-Shan suka
tafi Yabesh inda suka ƙone su. 13 Sai suka kwashi ƙasusuwansu suka binne a gindin
itace tsamiya a Yabesh, suka kuma yi azumi kwana bakwai.

# 2 Sama’ila

*Dawuda ya ji labarin mutuwar Shawulu*

1 Bayan mutuwar Shawulu, Dawuda ya dawo daga karkashe Amalekawa. Sai ya
zauna a Ziklag kwana biyu. 2 A rana ta uku sai ga wani mutum ya zo daga sansanin
Shawulu da yagaggen riga da ƙura a kansa. Da ya zo wurin Dawuda sai ya fāɗi a
ƙasa don yǎ nuna bangirma.
3 Dawuda ya tambaye shi ya ce, “Daga ina ka fito?”
Ya amsa ya ce, “Na tsere ne daga sansanin Isra’ila.”
4 Dawuda ya ce, “Gaya mini, me ya faru?”
Sai ya ce, “Mutane sun gudu daga yaƙi, aka kuma karkashe yawancin mutane.
Shawulu da ɗansa Yonatan ma sun mutu.”
5 Sai Dawuda ya ce wa saurayin da ya kawo labarin, “Yaya ka san cewa Shawulu
da ɗansa Yonatan sun mutu?”
6 Saurayin ya ce, “Ina kan dutsen Gilbowa a lokacin sai na ga Shawulu jingine a
māshinsa. Kekunan yaƙi da mahayansu suna matsowa kusa da shi. 7 Da ya juya ya
gan ni sai ya kira ni, na kuwa ce masa, ‘Ga ni?’
8 “Ya tambaye ni ya ce, ‘Wane ne kai?’
“Na ce, ‘Ni mutumin Amalek ne.’
9 “Sai ya ce mini, ‘Matso kusa ka kashe ni! Ina cikin azabar mutuwa, sai dai har
yanzu ina da rai.’
10 “Saboda haka na matso kusa da shi na kashe shi, domin na san cewa ba zai yi
rai ba, da yake ya riga ya fāɗi. Sai na cire rawanin da yake kansa, na kuma cire
warwaron hannunsa, na kuwa kawo maka su duka, ranka yǎ daɗe!”
11 Sai Dawuda da dukan mutanen da suke tare da shi suka yayyage rigunarsu.
12 Suka yi makoki, da kuka, da azumi har yamma saboda Shawulu da ɗansa Yonatan,
da saboda sojojin Ubangiji, da kuma gidan Isra’ila, gama an karkashe su a yaƙi.
13 Dawuda ya ce wa saurayin da ya kawo labarin, “Daga ina ka fito?”
Ya ce, “Ni ɗan wani baƙo ne, mutumin Amalek.”
14 Dawuda ya ce masa, “Yaya ba ka ji tsoro ɗaga hannu ka hallaka shafaffe na
Ubangiji ba?”
15 Sai Dawuda ya kira ɗaya daga cikin mutanensa ya ce, “Je ka kashe shi!” Haka
kuwa ya buge shi, ya kuwa mutu. 16 Gama Dawuda ya riga ya ce masa, “Alhakin
jininka yana bisa kanka tun da yake da bakinka ka ce, ‘Ni ne na kashe shafaffe na
Ubangiji.’ ”

*Dawuda ya yi makokin Shawulu da Yonatan*

17 Dawuda ya rera wannan makoki saboda Shawulu da ɗansa Yonatan. 18 Ya umarta
a koya wa mutanen Yahuda wannan waƙa mai suna Makokin Baka (tana a rubuce a
Littafin Yashar),
19 “Ya Isra’ila, an kashe darajarki a kan tuddanki.
Ga shi, jarumawa sun fāɗi!

20 “Kada a faɗe shi a Gat,
kada a yi shelarsa a titunan Ashkelon,
don kada ’yan matan Filistiyawa su yi murna
don kada ’yan matan marasa kaciya su yi farin ciki.

21 “Ya duwatsun Gilbowa,

kada a sāke yin ruwa ko raɓa a kanku,
balle gonakin da suke ba da hatsin hadaya su ƙara bayarwa.
Gama a can ne garkuwoyin manyan sojoji suka kwanta,
suka kwanta a wulaƙance.
Garkuwar Shawulu kuwa,
ba za a ƙara shafa mata mai ba.

22 "Daga jinin waɗanda aka kashe,
daga tsokar naman jarumi,
bakan Yonatan bai juye baya ba,
takobin Shawulu bai komo ba tare da gamsuwa ba.
23 Shawulu da Yonatan,
a raye ƙaunatattu ne da kuma bansha'awa,
a mace kuma ba su rabu ba.
Sun fi gaggafa sauri,
sun fi zaki ƙarfi.

24 "Ya ku 'yan matan Isra'ila,
ku yi kuka saboda Shawulu,
wanda ya suturta ku da jajjayen kayan ado,
wanda ya yi wa rigunarku ado da zinariya.

25 "Jarumawa sun fāɗi a yaƙi!
Ga Yonatan matacce a tuddanku.
26 Na yi baƙin ciki saboda kai, Yonatan ɗan'uwana;
ƙaunatacce kake a gare ni.
Kaunarka a gare ni abar al'ajabi ce,
abar al'ajabi fiye da ta mace.

27 "Jarumawa sun fāɗi!
Makaman yaƙi sun hallaka!"

# 2

*An naɗa Dawuda sarki a kan Yahuda*

1 Bayan 'yan kwanaki, sai Dawuda ya nemi nufin UBANGIJI ya ce, "In haura zuwa
ɗaya daga cikin biranen Yahuda?"
UBANGIJI ya ce, "Haura."
Dawuda ya ce, "Wanne zan tafi?"
UBANGIJI ya ce, "Je Hebron."
2 Saboda haka sai Dawuda ya tafi can tare da matansa biyu, Ahinowam daga
Yezireyel da Abigiyel gwauruwar Nabal mutumin Karmel. 3 Dawuda kuma ya tafi
tare da dukan mutanen da suke tare da shi, kowa da iyalinsa, suka zauna a Hebron
da garuruwansa. 4 Sa'an nan mutanen Yahuda suka zo Hebron, a can kuwa suka
naɗa Dawuda sarkin Yahuda.
Sa'ad da aka gaya wa Dawuda cewa mutanen Yabesh Gileyad ne suka binne
Shawulu, 5 sai ya aiki manzanni zuwa Yabesh Gileyad a ce musu, "UBANGIJI yă
albarkace ku saboda alherin da kuka nuna wa Shawulu ta wurin binne shi. 6 Bari
UBANGIJI yă nuna muku ƙaunarsa da amincinsa, ni kuma zan nuna muku irin
wannan alherin saboda kun yi haka. 7 Yanzu fa, sai ku ƙarfafa, ku yi jaruntaka,
gama Shawulu sarkinku ya mutu, gidan Yahuda kuwa sun naɗa ni sarki a kansu."

*Yaƙi tsakanin gidan Dawuda da na Shawulu*

8 Ana cikin haka, Abner ɗan Ner, komandan sojojin Shawulu, ya ɗauki Ish-Boshet
ɗan Shawulu ya kawo shi Mahanayim. 9 Ya naɗa shi sarkin Gileyad, da na Ashuri*,
da na Yezireyel, da a kan Efraim, da Benyamin, da kuma na dukan Isra'ila.
10 Ish-Boshet ɗan Shawulu yana da shekaru arba'in sa'ad da ya zama sarkin Isra'ila,
ya kuma yi sarauta shekara biyu. Amma fa, gidan Yahuda, suka bi Dawuda. 11 Tsawon
lokacin da Dawuda ya yi mulki a Hebron a kan gidan Yahuda, shekara bakwai ne da
wata shida.
12 Abner ɗan Ner, tare da mutanen Ish-Boshet ɗan Shawulu, suka bar Mahanayim
suka tafi Gibeyon. 13 Yowab wanda ake ce mamarsa Zeruhiya tare da waɗansu
mutanen Dawuda suka fito suka haɗu da su tafkin Gibeyon, Suka zauna, waɗannan
a wannan gefe, waɗancan a wancan gefe.
14 Sa'an nan Abner ya ce wa Yowab, "Bari mu bar waɗansu samari su tashi su yi
faɗa hannu da hannu a gabanmu."
Yowab ya ce, "To, su tashi."
15 Saboda haka samarin suka tashi aka ƙidaya su, mutum sha biyu wajen Benyamin
da Ish-Boshet ɗan Shawulu, sha biyu kuma wajen Dawuda. 16 Sa'an nan kowannensu
ya kama abokin gābansa a kā ya soki da wuƙa a jiki, sai duka suka fāɗi a ƙasa.
Saboda haka ne ake kiran wannan wuri Helkat Hazzurim† a Gibeyon.
17 Faɗan ya yi zafi a ranar ƙwarai, mutanen Dawuda suka ci mutanen Abner da
na Isra'ila.
18 'Ya'yan Zeruhiya, maza uku sun kasance a can. Su ne, Yowab, Abishai da Asahel.
To, Asahel mai gudu ne kamar barewa. 19 Ya fafari Abner, bai juya dama ko hagu ba,
yayinda yake fafararsa. 20 Abner ya waiga, sai ya ce, "Kai ne, Asahel?"
Ya ce, "Ni ne."
21 Sai Abner ya ce masa, "Yi dama ko hagu ka runtumi ɗaya daga cikin samarin,
ka ƙwace makamansa." Amma Asahel bai bar fafararsa ba.
22 Abner ya sāke gargaɗe shi ya ce, "Ka bar fafarata! Yaya zan kashe ka? Yaya zan
yin ido biyu da ɗan'uwanka Yowab?"
23 Amma Asahel ya ƙi yǎ bar fafararsa; saboda haka Abner ya soki Asahel da
māshinsa a ciki; har māshin ya fita ta bayansa. Nan take ya fāɗi, ya mutu. Kowa da
ya zo wurin da Asahel ya fāɗi, ya mutu, sai yǎ tsaya.
24 Amma Yowab da Abishai suka fafari Abner, kuma da rana tana fāɗuwa sai suka
iso tudun Amma, kusa da Giya, a hanyar zuwa jejin Gibeyon. 25 Sa'an nan mutanen
Benyamin suka haɗa kansu suka koyi bayan Abner. Suka zama ƙungiya guda, suka
tsaya daram a kan tudu.
26 Sai Abner ya kira Yowab ya ce, har abada ne māshi zai yi ta hallakarwa? Ba
ka sani cewa ƙarshen zai zama da ɗaci ba. Sai yaushe za ka umarci mutanenka su
daina fafaran 'yan'uwansu?
27 Yowab ya ce, "Muddin Allah yana a raye, da ba a ce ka yi magana ba, da mutanen
za su ci gaba da fafaran 'yan'uwansu har gari yǎ waye."
28 Sai Yowab ya busa ƙaho, dukan mutane kuwa suka tsaya; suka daina fafaran
Isra'ila. Nan take faɗan ya tsaya.
29 Abner da mutanensa suka ratsa kwarin Urdun dukan dare. Sa'an nan suka haye
kogin, suka kuwa ci gaba dukan safe‡ har suka zo Mahanayim.
30 Da Yowab ya dawo daga fafaran Abner, sai ya tattara dukan mutanensa. Ban da
Asahel, sai ya gane an rasa mutum goma sha tara na Dawuda. 31 Amma mutanen
Dawuda sun kashe mutum ɗari uku da sittin daga kabilar Benyamin da suke tare

* **2:9** Ko kuwa Asher † **2:16** Helkat Hazzurim yana nufin filin wuƙaƙe ko filin rikici. ‡ **2:29** Ko kuwa safe; Ko kuwa rafi; ba a tabbatar da kalman nan ta Ibraniyawa ba.

da Abner. 32 Suka ɗauki gawar Asahel suka binne a kabarin mahaifinsa a Betlehem.
Sa'an nan Yowab da mutanensa suka bi dare har suka iso Hebron da safe.

# 3

*(1 Tarihi 3.1-4)*

1 Aka daɗe ana yaƙi tsakanin gidan Shawulu da gidan Dawuda. Dawuda kuwa ya
yi ta ƙara ƙarfi, yayinda gidan Shawulu ya yi ta raguwa a ƙarfi.

2 An haifa wa Dawuda 'ya'ya maza a Hebron.

Ɗansa na fari shi ne Amnon, ɗan Ahinowam mutuniyar Yezireyel;
3 na biyu shi ne Kileyab, ɗan Abigiyel gwauruwar Nabal mutumin Karmel;
na uku shi ne Absalom, ɗan Ma'aka 'yar Talmai sarkin Geshur;
4 na huɗu shi ne Adoniya, ɗan Haggit;
na biyar shi ne Shefatiya, ɗan Abital;
5 na shida kuma shi ne Itireyam, ɗan Egla matar Dawuda.

An haifi waɗannan wa Dawuda a Hebron.

*Abner ya koma ɓangaren Dawuda*

6 Sa'ad da ake yaƙi tsakanin gidan Shawulu da gidan Dawuda, sai Abner ya yi ta
ƙarfafa matsayinsa a gidan Shawulu. 7 To, Shawulu yana da ƙwarƙwarar da ake kira
Rizfa, 'yar Aiya. Sai Ish-Boshet ya ce wa Abner, "Don me kake kwana da ƙwarƙwarar
mahaifina?"
8 Abner ya husata saboda abin da Ish-Boshet ya ce, sai ya ce, "Kana tsammani ni
mai cin amana ne? Kana zato ni mai goyon bayan Yahuda ne? Tun farko na nuna
aminci ga gidan babanka Shawulu, da 'yan'uwansa, da abokansa! Ban kuwa ba da
kai a hannun Dawuda ba. Ga shi yanzu a kan mace za ka ga laifina? 9 Allah yǎ yi
wa Abner hukunci mai tsanani, in ban goyi bayan Dawuda ya sami abin da UBANGIJI
ya yi masa alkawari da rantsuwa ba. 10 Zan kuma mayar wa Dawuda sarautar gidan
Shawulu, in kafa kursiyin Dawuda a kan Isra'ila, da kan Yahuda tun daga Dan har
zuwa Beyersheba." 11 Ish-Boshet bai ƙara yin karambanin ce wa Abner kome ba,
gama yana tsoronsa.
12 Sai Abner ya aiki manzanni a madadinsa wurin Dawuda su ce masa, "Kasar ta
wane ne? Ka yi yarjejjeniya da ni, zan kuwa taimake ka, in juye dukan Isra'ila zuwa
ɓangarenka."
13 Dawuda ya ce, "Da kyau, zan yi yarjejjeniya da kai, amma fa ina bukata abu
guda daga gare ka, kada ka zo gabana in ba tare da matata Mikal, 'yar Shawulu ba."
14 Sai Dawuda ya aiki manzanni zuwa wurin Ish-Boshet ɗan Shawulu cewa, "Ka ba
ni matata Mikal wadda na biya sadakinta da loɓa ɗari na Filistiyawa."
15 Sai Ish-Boshet ya ba da umarni, aka kuwa ɗauke ta daga gidan mijinta Faltiyel
ɗan Layish. 16 Amma mijin ya raka ta, yana tafe yana kuka, ya bi ta har Bahurim.
Sai Abner ya ce masa, "Koma gida!" Sai ya koma.
17 Abner ya tattauna da dattawan Isra'ila ya ce, "An daɗe kuna nema ku naɗa
Dawuda sarkinku. 18 To, yanzu sai ku yi haka! Gama UBANGIJI ya yi wa Dawuda
alkawari ya ce, 'Ta wurin bawana Dawuda zan ceci mutanena Isra'ila daga hannun
Filistiyawa, da kuma hannun dukan abokan gābansu.' "
19 Abner kuma ya yi magana da mutane Benyamin da kansa. Sa'an nan ya tafi
Hebron yǎ gaya wa Dawuda ko mene ne Isra'ila da kuma dukan gidan Benyamin
suke so su yi. 20 Sa'ad da Abner wanda yake tare da mutane ashirin suka zo wurin
Dawuda a Hebron, Dawuda ya shirya masa liyafa tare da mutanensa. 21 Sai Abner ya

ce wa Dawuda, "Bari in tafi nan da nan in tattara dukan Isra'ila wa ranka yă daɗe, sarki, saboda su yi alkawari da kai, ka kuma ka yi mulki bisa dukansu yadda ranka yake so." Saboda haka Dawuda ya sallami Abner, ya kuwa tafi lafiya.

### *Yowab ya kashe Abner*

22 Ba a jima ba sai mutanen Dawuda da Yowab suka dawo daga hari. Suka kawo
ganima da yawa tare da su. Abner kuwa ya riga ya bar Dawuda a Hebron, domin
Dawuda ya sallame shi, shi kuma ya tafi lafiya. 23 Sa'ad da Yowab da dukan sojoji
suka dawo, aka gaya masa cewa Abner ɗan Ner ya zo wurin sarki, sarki kuwa ya
sallame shi, ya kuma tafi lafiya.
24 Sai Yowab ya je wurin sarki ya ce, "Me ke nan ka yi? Abner ya zo wurinka. Don
me ka ƙyale shi yă tafi? Ga shi kuwa ya tafi! 25 Ka san Abner ɗan Ner ya zo ne yă
ruɗe ka, yă ga fitarka da shigarka, yă kuma binciki kome da kake yi."
26 Yowab ya tashi daga gaban Dawuda ya tafi ya aika manzanni su bi Abner. Suka
same shi a rijiyar Sira suka komo da shi, Dawuda kuwa bai sani ba. 27 To, da Abner
ya komo Hebron, Yowab ya ratse da shi zuwa hanyar shigar gari kamar zai gana da
shi a kaɗaice. Amma a can ya soki Abner a ciki, ya kashe shi don yă rama mutuwar
ɗan'uwansa Asahel.
28 Daga baya, Dawuda ya ji labarin sai ya ce, "Ni da masarautata har abada ba mu
da laifi a gaban UBANGIJI game da jinin Abner ɗan Ner. 29 Alhakin jininsa yă kasance
a kan Yowab da kuma a kan dukan iyalin mahaifinsa! Kada gidan Yowab yă rasa mai
ɗiga, ko kuturu, ko mai jingina ga sanda, ko wanda aka kashe da takobi, ko kuma
wanda ba shi da abinci."
30 (Yowab da ɗan'uwansa Abishai suka kashe Abner don yă kashe ɗan'uwansu
Asahel a yaƙin Gibeyon.)
31 Sa'an nan Dawuda ya ce wa Yowab da dukan mutanen da suke tare da shi, "Ku
yayyage rigunarku, ku sa tsummoki, ku yi tafiya kuna kuka a gaban Abner." Sarki
Dawuda kansa ya bi masu ɗauke da gawar daga baya. 32 Suka binne Abner a Hebron,
sarki kuwa ya ɗaga murya ya yi kuka a kabarin Abner.
33 Sarki ya kuma yi wannan waƙar makoki domin Abner ya ce,

"Daidai ne Abner yă mutu, kamar yadda marasa bin doka suke mutuwa?
34 Hannuwanka ba a daure suke ba,
ƙafafunka ba a tabaibaye suke ba.
Ka mutu kamar waɗanda suke mutuwa a hannun mugaye."

Sai dukan mutane suka sāke fashe da kuka saboda shi.
35 Sa'an nan duk suka zo suka roƙi Dawuda yă ci wani abu tun rana ba tă fāɗi ba;
amma Dawuda ya rantse ya ce, "Bari Allah yă hukunta ni, in na ɗanɗana abinci ko
wani abu kafin rana ta fāɗi!"
36 Dukan mutane suka lura suka kuma ji daɗi ƙwarai, tabbatacce kome da sarki ya
yi, ya gamshe su. 37 Saboda haka a ranar dukan mutane da dukan Isra'ila suka gane
sarki ba shi da hannu a kisan Abner ɗan Ner.
38 Sa'an nan sarki ya ce wa mutanensa, "Ba ku gane cewa ɗan sarki kuma babban
mutum ya mutu a ƙasar Isra'ila a yau ba? 39 A yau, ko da yake ni naɗaɗɗen sarki ne,
duk da haka na raunana, kuma waɗannan 'ya'yan Zeruhiya sun fi ƙarfina. UBANGIJI
yă sāka wa mai aikata mugunta da muguntar da ya aikata!"

## 4

### *An kashe Ish-Boshet*

1 Sa'ad da Ish-Boshet ya ji labari cewa Abner ya mutu a Hebron, sai ya karaya,
sai dukan hankalin Isra'ila ya tashi. 2 To, ɗan Shawulu yana da 'ya'ya maza biyu
da suke shugabannin 'yan hari. Ana kiran ɗaya Ba'ana, ɗayan kuma Rekab. Su

'ya'yan Rimmon mutumin Benyamin ne daga Beyerot, an lissafta Beyerot a ɓangaren
Benyamin, 3 domin mutanen Beyerot sun gudu zuwa Gittayim inda suke zaman
baƙunci har wa yau.

4 (Yonatan ɗan Shawulu yana da ɗa mai suna Mefiboshet wanda yake gurgu a duka
ƙafafu. Yana da shekara biyar ne sa'ad da labarin mutuwar Shawulu da Yonatan ya
zo daga Yezireyel. Sai mai renonsa ta ɗauke shi ta gudu, amma yayinda take hanzari
tă gudu, sai ya fāɗo, ya gurgunce.)

5 To, Rekab da Ba'ana, 'ya'yan Rimmon mutumin Beyerot, suka tafi gidan Ish-
Boshet, suka isa can da tsakar rana yayinda yake hutun tsakar rana. 6 Suka shiga
sashe na cikin gida sai ka ce suna so su ɗibo alkama ne, suka soke shi a ciki. Sa'an
nan Rekab da Ba'ana ɗan'uwansa suka zame suka ɓace.

7 Sun shiga gidan yayinda yake kwance a gado a ɗakin barcinsa. Bayan sun soke
shi sai suka kashe shi, suka kuma datse kansa. Suka ɗauke shi, suka yi tafiya dukan
dare suka bi ta Araba. 8 Suka kawo kan Ish-Boshet wa Dawuda a Hebron, suka ce wa
sarki, "Ga kan Ish-Boshet ɗan Shawulu, maƙiyinka, wanda ya nemi yă kashe ka. A
yau UBANGIJI ya rama wa ranka yă daɗe sarki, a kan Shawulu da zuriyarsa."

9 Dawuda ya ce wa Rekab da ɗan'uwansa Ba'ana, 'ya'yan Rimmon mutumin
Beyerot, "Muddin UBANGIJI yana a raye, wanda ya kuɓutar da ni daga wahala, 10 sa'ad
da wani mutum ya ce mini, 'Shawulu ya mutu,' yana tsammani ya kawo labari mai
daɗi ne, na kama shi na kashe a Ziklag. Ladar da na ba shi ke nan saboda labarinsa!
11 Balle fa, sa'ad da mugayen mutane suka kashe marar laifi a gidansa, a bisa gadonsa,
ashe, ba zan nemi jininsa daga hannunku in kawar da ku a duniya ba!"

12 Saboda haka Dawuda ya umarci mutanensa, suka kuwa kashe su. Suka yayyanka
hannuwansu da ƙafafunsu, suka kuma rataye jikunansu kusa da tafki a Hebron.
Amma suka ɗauki kan Ish-Boshet suka binne a kabarin Abner a Hebron.

# 5

*Dawuda ya zama sarki a bisa Isra'ila*
*(1 Tarihi 11.1-3)*

1 Dukan kabilar Isra'ila suka zo wurin Dawuda a Hebron suka ce, "Mu nama da
jininka ne. 2 A dā da Shawulu yake sarauta a bisanmu, kai ne kake bi Isra'ilawa zuwa
yaƙe-yaƙensu. UBANGIJI kuwa ya ce maka, 'Za ka zama makiyayi mutanena Isra'ila,
za ka kuma zama sarkinsu.' "

3 Sa'ad da dukan dattawan Isra'ila suka zo wurin Sarki Dawuda a Hebron, sarki ya
yi yarjejjeniya da su a gaban UBANGIJI, suka kuwa naɗa Dawuda sarki bisa Isra'ila.

4 Dawuda yana da shekara talatin ɗaya sa'ad da ya zama sarki, ya kuma yi mulki
shekara arba'in. 5 A Hebron ya yi mulki a bisa Yahuda shekara bakwai da wata shida,
a Urushalima kuma ya yi mulki a bisa Isra'ila da Yahuda shekara talatin da uku.

*Dawuda ya kame Urushalima*
*(1 Tarihi 11.4-9; 14.1,2)*

6 Sarki da mutanensa suka tafi Urushalima don su kai wa Yebusiyawan da suke
zaune a can hari, Yebusiyawa suka ce wa Dawuda, "Ba za ka shiga nan ba; ko makafi
da guragu kaɗai ma za su kore ka." Suka yi tsammani suna cewa, "Dawuda ba zai
iya shiga can ba." 7 Duk da haka, Dawuda ya kame kagarar Sihiyona, wadda ta zama
Birnin Dawuda.

8 A ranar, Dawuda ya ce, "Duk wanda zai kame Yebusiyawa, dole yă yi amfani da
wuriyar ruwa don yă kai ga waɗannan 'guragu da makafi' waɗanda suke abokan
gāban Dawuda." Shi ya sa suka ce, " 'Makafi da guragu' ba za su shiga fadan sarki
ba."

[9] Sai Dawuda ya zauna a kagarar, ya kuma kira ta Birnin Dawuda. Ya gina wuraren
da suke kewaye da ita, tun daga madogaran gini* zuwa ciki. [10] Ya yi ta ƙara ƙarfi,
gama UBANGIJI Allah Maɗaukaki yana tare da shi.
[11] To, Hiram sarkin Taya ya aiki manzanni wurin Dawuda tare da gumaguman
itacen al'ul, da kafintoci, da kuma maginan duwatsu, suka kuwa gina wa Dawuda
fada. [12] Dawuda kuwa ya gane UBANGIJI ya naɗa shi sarki bisa Isra'ila, ya kuma
ɗaukaka masarautarsa saboda mutanensa Isra'ila.

*(1 Tarihi 14.3-7)*

[13] Bayan ya bar Hebron, Dawuda ya ƙara ɗauko wa kansa waɗansu ƙwarƙwarai
da mata a Urushalima. Aka haifa masa 'ya'ya maza da mata. [14] Waɗannan su ne
sunayen 'ya'yan da aka haifa masa a can. Shammuwa, Shobab, Natan, Solomon,
[15] Ibhar, Elishuwa, Nefeg, Yafiya, [16] Elishama, Eliyada da Elifelet.

### *Dawuda ya ci Filistiyawa da yaƙi*
*(1 Tarihi 14.8-17)*

[17] Da Filistiyawa suka ji labari an shafe Dawuda sarki a bisa Isra'ila, sai suka
haura da ƙarfi sosai don su nema shi, amma Dawuda ya ji labarin sai ya gangara
zuwa mafaka. [18] To, fa, Filistiyawa suka zo suka baje ko'ina a cikin Kwarin Refayim;
[19] saboda haka Dawuda ya nemi nufin UBANGIJI ya ce, "In tafi in kai wa Filistiya hari?
Za ka bashe su a hannuna?"

UBANGIJI ya amsa masa ya ce, "Je ka, gama tabbatacce zan bashe Filistiyawa a
hannunka."

[20] Saboda haka Dawuda ya tafi Ba'al-Ferazim, a can ya ci su da yaƙi. Sai ya
ce, "Kamar yadda ruwa yakan fasu, haka UBANGIJI ya kakkarya abokan gābana
a gabana." Saboda haka aka kira wurin Ba'al-Ferazim.† [21] Filistiyawa suka bar
gumakansu a can, Dawuda da mutanensa kuwa suka kwashe su.
[22] Har yanzu Filistiyawa suka sāke haurawa suka bazu a Kwarin Refayim; [23] saboda
haka Dawuda ya nemi nufin UBANGIJI, ya kuwa ce, "Kada ka haura kai tsaye, amma
ka kewaya ta bayansu ka fāɗa musu a gaban itatuwan balsam. [24] Da zarar ka ji
tafiya kamar na takawar sojoji tana a bisan itatuwan balsam, sai ka yi maza, gama
wannan alama ce cewa UBANGIJI ya sha gabanka don yǎ karkashe sojojin Filistiyawa."
[25] Saboda haka Dawuda ya aikata yadda UBANGIJI ya umarce shi, ya kuma karkashe
Filistiyawa tun daga Geba har zuwa Gezer.

# 6

### *An kawo akwatin alkawari a Urushalima*
*(1 Tarihi 13.1-14; 15.1–16.3,43)*

[1] Dawuda ya sāke tattara zaɓaɓɓun mutanen Isra'ila, dubu talatin. [2] Shi, da dukan
mutanensa suka tashi daga Ba'ala-Yahuda* don su hauro da akwatin alkawarin
Allah, wanda ake kira da Sunan†UBANGIJI Maɗaukaki, wanda yake zama a tsakanin
kerubobin da suke a kan akwatin alkawarin. [3] Suka ɗauko akwatin alkawarin Allah
a sabuwar keken yaƙi, suka kawo shi daga gidan Abinadab, wanda yake bisa tudu.
Uzza da Ahiyo, 'ya'yan Abinadab maza, suka bi da keken yaƙin da akwatin alkawarin
Allah yake ciki suka bi da keken yaƙin [4] da akwatin alkawarin Allah yake ciki‡. Ahiyo
kuwa yana tafiya a gaban Abinadab. [5] Dawuda da dukan gidan Isra'ila suka yi biki

---

* **5:9** Ko kuwa Millo † **5:20** Ba'al-Ferazim yana nufin mai girma wanda ya kakkarya. * **6:2** Wato, Kiriyat Yeyarim; da Ibraniyanci Ba'ale Yahuda, wani sunan Ba'ala-Yahuda. † **6:2** Ibraniyanci; Seftuwajin da kuma Bulget ba su da Suna. ‡ **6:4** Naɗaɗɗun littattafan Mataccen Teku da waɗansu rubuce-rubucen hannu na Seftuwajin; Nassin Masoretik amalanke 4 suka kuma kawo shi tare da akwatin alkawarin Allah daga gidan Abinadab, wanda yake a kan tudu

sosai da dukan ƙarfinsu a gaban Ubangiji, da waƙoƙi,§ da molaye, da garayu, da ganguna, da kacau-kacau da kuma kuge.
6 Da suka kai masussukar Nakon, sai Uzza ya miƙa hannu don yă riƙe akwatin alkawarin Allah, gama shanun sun yi tuntuɓe.
7 Fushin Ubangiji kuwa ya ƙuna a kan Uzza domin aikin rashin bangirma, saboda haka Allah ya buge shi ya kuma mutu a can kusa da akwatin alkawarin Allah.
8 Ran Dawuda ya ɓace gama fushin Ubangiji ya ɓarke a kan Uzza. Shi ya sa har wa yau ana kira wurin Ferez Uzza.*
9 Dawuda ya ji tsoron Ubangiji a ranar, sai ya ce, "Yaya akwatin alkawarin Ubangiji zai iya zuwa wurina?"
10 Bai so yă ɗauki akwatin alkawarin Ubangiji yă kasance tare da shi a Birnin Dawuda ba. A maimakon haka sai ya kai shi gidan Obed-Edom mutumin Gat.
11 Akwatin Alkawarin Ubangiji ya kasance a gidan Obed-Edom mutumin Gat har tsawon wata uku, Ubangiji kuwa ya albarkace shi da dukan iyalinsa.
12 To, sai aka faɗa wa Sarki Dawuda cewa, "Ubangiji ya sa wa gidan Obed-Edom albarka da dukan abin da yake da shi, saboda akwatin alkawarin Allah." Saboda haka sai Dawuda ya gangara ya hauro da akwatin alkawarin Allah daga gidan Obed-Edom zuwa Birnin Dawuda da farin ciki.
13 Sa'ad da waɗanda suke ɗaukan akwatin alkawarin Ubangiji suka yi tafiya taki shida, sai yă yi hadayar bijimi da saniya mai ƙiba.
14 Dawuda, sanye da efod lilin, ya yi ta rawa a gaban Ubangiji da dukan ƙarfinsa,
15 yayinda shi da dukan gidan Isra'ila suka hauro da akwatin alkawarin Ubangiji da sowa da kuma busar ƙahoni.
16 Sa'ad da akwatin alkawarin Ubangiji ya shiga Birnin Dawuda, sai Mikal 'yar Shawulu ta leƙa ta taga ta ga Dawuda sarki yana tsalle, yana rawa a gaban Ubangiji, sai ta rena shi a zuciyarta.
17 Suka kawo akwatin alkawarin Ubangiji, aka ajiye shi a inda aka shirya masa a cikin tentin da Dawuda ya shirya dominsa. Dawuda kuma ya miƙa hadaya ta ƙonawa da hadaya ta salama a gaban Ubangiji.
18 Bayan ya gama yin hadaya ta ƙonawa da hadaya ta salama, sai ya albarkaci mutane a cikin sunan Ubangiji Maɗaukaki.
19 Sa'an nan ya rarraba abinci, da ƙosai, dabino, da waina ga kowane mutum a cikin dukan jama'ar Isra'ila, maza da mata. Dukan mutane kuwa suka watse zuwa gidajensu.
20 Da Dawuda ya koma gida don yă sa wa gidansa albarka, sai Mikal 'yar Shawulu ta fito don tă tarye shi, sai ta ce, "Tabbas sarkin Isra'ila ya fiffita kansa yau, ya tuɓe a gaban bayinsa 'yan mata, kamar yadda duk marar kunya yakan yi!"
21 Dawuda ya ce wa Mikal, "Na yi rawana domin in girmama Ubangiji ne, wanda ya zaɓe ni a maimakon mahaifinki ko wani daga cikin dukan gidansa, shi ne kuma ya sa ni sarki a kan Isra'ila, mutanen Ubangiji, zan yi biki a gaban Ubangiji.
22 Zan ma mai da kaina abin reni fiye da haka, za a kuma zama abin reni a gare ki. Amma waɗannan bayi 'yan matan da kika yi magana a kai, za su gan ni da martaba."
23 Mikal 'yar Shawulu kuwa ba tă haifi ɗa ba har mutuwarta.

# 7

*Alkawarin Allah ga Dawuda*
*(1 Tarihi 17.1-15)*

1 Bayan sarki ya kama zama a fadansa Ubangiji kuma ya hutashe shi daga dukan abokan gābansa da suke kewaye da shi,
2 sai ya ce wa annabi Natan, "Ga ni, ina zama a fadar katakon al'ul, amma akwatin alkawarin Allah yana zaune a tenti."

§ **6:5** Dubi Littattafan Mataccen Teku, Seftuwajin da 1Tar 13.8; Nassin Masoretik biki a gaban Ubangiji da kowane irin kayan kiɗin da aka yi da fir. * **6:8** Ferez Uzza yana nufin ɓarke a kan Uzza.

[3] Natan ya amsa wa sarki ya ce, "Duk abin da yake a zuciyarka, sai ka yi, gama
UBANGIJI yana tare da kai."
[4] A daren nan maganar UBANGIJI ta zo wa Natan cewa,
[5] "Je ka faɗa wa bawana Dawuda, 'Ga abin da UBANGIJI ya ce, kai ne za ka gina
mini gida in zauna? [6] Ban taɓa zama a gida ba tun daga ranar da na fito da
Isra'ilawa daga Masar har yă zuwa yau. Ina dai kai da kawowa a tenti, a matsayin
mazaunina. [7] A cikin kaiwa da kawowar da nake yi cikin dukan Isra'ilawa, na taɓa
ce wa wani shugabanninsu wanda na umarta su lura da mutanena Isra'ila, "Don
me ba ku gina mini mazauni da katakon al'ul ba?" '
[8] "Yanzu, ka gaya wa bawana Dawuda 'Ga abin da UBANGIJI Maɗaukaki ya ce, na
ɗauko ka daga makiyaya, daga kuma garken tumaki ka zama sarki bisan mutane
Isra'ila. [9] Na kasance tare da kai duk inda ka tafi, na kuma kawar da dukan abokan
gābanka a gabanka. Yanzu zan sa sunanka yă shahara kamar sunayen shahararrun
mutanen duniya. [10] Zan kuma tanada wa mutanena Isra'ila wuri, in kuma dasa su
yadda za su kasance da gida kansu ba tare da an ƙara damunsu ba. Mugayen
mutane ba za su ƙara wahalshe su kamar dā ba, [11] yadda suka yi tun lokacin da
na naɗa shugabanni bisan mutanena Isra'ila, zan kuma hutashe ka daga hannun
abokan gābanka.
" 'UBANGIJI ya furta maka cewa UBANGIJI kansa zai kafa maka gida. [12] Sa'ad da
kwanakinka suka ƙare, za ka huta tare da kakanninka, zan tā da zuriyarka, na
cikinka, zan kuma sa mulkinsa ya kahu. [13] Shi zai gina gida domin Sunana, zan
kuwa kafa gadon sarautarsa har abada. [14] Zan zama Ubansa, shi kuma yă zama
ɗana. Idan ya yi laifi, zan yi amfani da mutane in hukunta shi. Mutane ne za su
zama bulalata. [15] Amma ba za a taɓa ɗauke ƙaunata daga gare shi yadda na ɗauke
ta daga wurin Shawulu ba, shi wannan wanda na kawar daga gabanka. [16] Gidanka
da kuma masarautarka za su dawwama har abada a gabana; gadon sarautarka
kuma zai kahu har abada.' "
[17] Natan ya gaya wa Dawuda dukan abin da Allah ya bayyana masa.

### *Addu'ar Dawuda*
### *(1 Tarihi 17.16-27)*

[18] Sa'an nan Sarki Dawuda ya je ya zauna a gaban UBANGIJI ya ce,
"Wane ne ni, ya UBANGIJI Mai Iko Duka, ko gidana, har da ka ɗaga mu zuwa
wannan matsayi? [19] Har ya zama kamar wannan bai isa ba a gabanka, ya UBANGIJI
Mai Iko Duka, ka kuma yi magana game da nan gaba na gidan bawanka. Haka ka
saba yi da mutane, ya UBANGIJI Mai Iko Duka?
[20] "Me kuma Dawuda zai ce maka? Gama ka san bawanka, ya UBANGIJI Mai Iko
Duka. [21] Gama saboda maganarka da kuma bisa ga nufinka, ka aikata wannan
babban abu, ka kuma sanar da bawanka.
[22] "Kai mai girma ne, ya UBANGIJI Mai Iko Duka! Babu wani kamar ka, babu
kuma wani Allah sai kai; kamar yadda muka ji da kunnuwanmu. [23] Wane ne kuma
yake kamar da mutanenka Isra'ila, al'umma guda a duniya wadda Allah ya fita
don yă kuɓutar wa kansa, ya kuma yi suna wa kansa, ya kuma aikata manyan
abubuwa da kuma al'amuran banmamaki ta wurin korin al'ummai da allolinsu
daga gaban mutanenka, waɗanda ka kuɓutar daga Masar?* [24] Ka kafa mutanenka
Isra'ila kamar naka na kanka har abada, kai kuma, ya UBANGIJI, ka zama Allahnsu.
[25] "Yanzu kuwa, ya UBANGIJI Allah, ka cika alkawarin da ka yi game da bawanka
da gidansa. Ka yi kamar yadda ka alkawarta, [26] domin sunanka yă kasance da

* **7:23** Dubi Seftuwajin da kuma 1Tar 17.21; Ibraniyanci abubuwan banmamaki domin ƙasarka da kuma a gaban mutanenka, waɗanda ka kuɓutar daga Masar, daga al'ummai da allolinsu.

girma har abada. Sa'an nan mutane za su ce, 'UBANGIJI Maɗaukaki, Allah ne a bisa
Isra'ila!' Kuma gidan bawanka Dawuda zai kahu a gabanka.
27 "Ya UBANGIJI Maɗaukaki, Allah na Isra'ila, ka bayyana wa bawanka cewa, 'Zan
gina maka gida.' Saboda haka bawanka ya sami ƙarfin hali yă miƙa maka wannan
addu'a. 28 Ya UBANGIJI Mai Iko Duka, kai Allah ne! Maganarka da aminci take, ka
kuma yi wa bawanka waɗannan abubuwa masu kyau. 29 In ya gamshe ka, bari
ka albarkaci gidan bawanka don yă dawwama a gabanka har abada; gama kai, ya
UBANGIJI Mai Iko Duka, ka riga ka yi magana, kuma saboda kai ka sa albarka ga
gidan bawanka, lalle zai kasance da albarka har abada."

# 8

*Nasarorin Dawuda*
*(1 Tarihi 18.1-13)*

1 Ana nan, sai Dawuda ya ci Filistiyawa da yaƙi, ya kawo ƙarshen mulkinsu a ƙasar,
ya kuma ƙwace ƙasar Meteg Amma daga hannun Filistiyawa.
2 Haka kuma Dawuda ya ci Mowabawa. Ya sa suka kwanta a ƙasa, ya kuma auna
su da igiya. Kowane awo biyu ya sa a kashe su, amma awo na uku sai yă sa a bar su
da rai. Saboda haka Mowabawa suka zama bayin Dawuda, suka kuma kawo masa
haraji.
3 Ban da haka, Dawuda ya yaƙi Hadadezer ɗan Rehob, sarkin Zoba. Wannan ya
faru a lokacin da Hadadezer yake kan hanyarsa zuwa Kogin Yuferites don yă sāke
mai da wurin a ƙarƙashin ikonsa. 4 Dawuda ya kame keken yaƙinsa guda dubu,
mahayan keken yaƙinsa dubu bakwai*, da sojojin ƙasa dubu ashirin. Ya yayyanke
agaran dawakan duka amma ya bar dawakai kekunan yaƙi ɗari.
5 Sa'ad da Arameyawan Damaskus suka zo don su taimaki Hadadezer sarkin Zoba,
sai Dawuda ya karkashe dubu ashirin da biyunsu. 6 Ya ajiye ƙungiyoyi sojoji a
masarautar Arameyawan Damaskus, Arameyawa kuwa suka zama bayinsa, suka biya
shi haraji. UBANGIJI ya ba Dawuda nasara a duk inda ya tafi.
7 Dawuda ya kwashe garkuwoyin zinariya na shugabannin sojojin Hadadezer ya
kawo Urushalima. 8 Daga Teba† da Berotai, garuruwan da suke ƙarƙashin Hadadezer,
Sarki Dawuda ya kwashe tagulla masu yawan gaske.
9 Da Towu‡ sarkin Hamat ya ji cewa Dawuda ya ci dukan rundunar Hadadezer, 10 sai
ya aiki ɗansa Yoram§ wurin Sarki Dawuda yă gaishe, yă kuma yi masa barka saboda
nasarar da ya yi a kan Hadadezer, gama Hadadezer nan ya hana Towu sakewa. Yoram
ya tafi ɗauke da kayan azurfa, da na zinariya, da na tagulla.
11 Sarki Dawuda kuwa ya keɓe waɗannan kayayyaki wa UBANGIJI, yadda ya yi da
zinariya, da kuma azurfa daga dukan al'umman da ya mallaka, 12 wato, azurfa da
zinariyan mutanen Edom, da na Mowabawa, da na Ammonawa, da na Filistiyawa,
da na Amalekawa, da ganimar Hadadezer ɗan Rehob, sarkin Zoba.
13 Dawuda kuwa ya ƙara zama shahararre bayan ya dawo daga kai wa ƙasar Aram
hari, daga nan sai ya je ya karkashe mutanen Edom* dubu goma sha takwas a Kwarin
Gishiri.
14 Ya ajiye rundunar sojoji ko'ina a Edom, dukan mutanen Edom kuwa suka zama
bayin Dawuda. UBANGIJI ya ba wa Dawuda nasara a duk inda ya tafi.

* **8:4** Seftuwajin (duba kuma Naɗaɗɗun Littattafan Matacce Teku da kuma 1Tar 18.4); Nassin Masoretik kame mahayan keken yaƙinsa ɗari goma sha bakwai † **8:8** Dubi waɗansu rubuce-rubucen hannun Seftuwajin (dubi kuma 1Tar 18.8); Ibraniyanci Beta. ‡ **8:9** Da Ibraniyanci Toi, wani suna na Towu; haka ma a aya 10. § **8:10** Wani suna na Hadoram * **8:13** Kaɗan a cikin rubuce-rubucen hannu na Ibraniyanci, Seftuwajin da kuma Siriyak (dubi kuma 1Tar 18.12); yawancin rubuce-rubucen hannu na Ibraniyanci suna da Aram (wato, Arameyawa).

*Hafsoshin Dawuda*
*(1 Tarihi 18.14-17)*

15 Dawuda ya yi mulkin dukan ƙasar Isra'ila, yana yin wa dukan jama'arsa shari'ar
gaskiya da adalci. 16 Yowab ɗan Zeruhiya ya zama shugaban sojoji; Yehoshafat ɗan
Ahilud kuwa shi ne marubucin tarihi; 17 Zadok ɗan Ahitub da Ahimelek ɗan Abiyatar,
su ne firistoci; Serahiya kuma sakatare; 18 Benahiya ɗan Yehohiyada ne shugaban
Keretawa da Feletiyawa, wato, sojoji masu gadin Dawuda, sa'an nan 'ya'yan Dawuda
maza su ne mashawartan sarki.†

# 9

*Dawuda da Mefiboshet*

1 Wata rana Dawuda ya yi tambaya ya ce, "Akwai wani har yanzu da ya rage a
gidan Shawulu wanda zan nuna masa alheri saboda Yonatan?"

2 To, akwai wani bawa na gidan Shawulu mai suna Ziba. Sai aka kira shi yǎ bayyana
a gaban Dawuda, sarki ya ce masa, "Kai ne Ziba?"

Sai ya ce, "I, ni ne, ranka yǎ daɗe."

3 Sa'an nan sarki ya yi tambaya ya ce, "Babu wani har yanzu da ya rage a gidan
Shawulu don in nuna masa alherin Allah?"

Ziba ya ce wa sarki, "Har yanzu akwai ɗan Yonatan da ya rage, sai dai shi gurgu
ne a dukan ƙafafu."

4 Sarki ya ce, "Ina yake?"

Ziba ya ce, "Yana a gidan Makir ɗan Ammiyel a Lo Debar."

5 Saboda haka Sarki Dawuda ya umarta aka kawo shi daga gidan Makir ɗan
Ammiyel, daga Lo Debar.

6 Sa'ad da Mefiboshet ɗan Yonatan, ɗan Shawulu, ya zo wurin Dawuda, sai ya
rusuna har ƙasa ya yi gaisuwar bangirma.

Dawuda ya ce, "Mefiboshet!"

Shi kuwa ya amsa ya ce, "Ranka yǎ daɗe, ga ni, bawanka."

7 Dawuda ya ce, "Kada ka ji tsoro, gama tabbatacce zan nuna maka alheri saboda
mahaifinka Yonatan. Zan mayar maka da dukan ƙasar da take ta kakanka Shawulu,
kullum kuma za ka ci a teburina."

8 Mefiboshet ya rusuna ya ce, "Ni ne wa har da za ka kula da ni? Ai! Ni bawanka
ne da bai ma fi mataccen kare daraja ba."

9 Sai sarki ya kira Ziba bawan Shawulu, ya ce masa, "Na ba wa jikan maigidanka
kome da yake na Shawulu da iyalinsa 10 Kai da 'ya'yanka maza da bayinka za ku
riƙa yin masa noma, ku kuma kawo hatsin, don jikan maigidanka yǎ sami abinci.
Mefiboshet kuma, jikan maigidanka, zai riƙa ci a teburina." (Ziba kuwa yana da
'ya'ya maza goma sha biyar da kuma bayi ashirin.)

11 Sai Ziba ya ce wa sarki, "Bawanka zai aikata dukan abin da ranka yǎ daɗe sarki,
ya umarce shi." Saboda haka Mefiboshet ya riƙa ci a teburin Dawuda kamar sauran
'ya'yan sarki.

12 Mefiboshet yana da wani ƙaramin ɗa sunansa Mika, dukan iyalin gidan Ziba
kuwa bayin Mefiboshet ne. 13 Mefiboshet ya zauna a Urushalima, gama kullum yana
ci a teburin sarki, shi kuwa gurgu ne a dukan ƙafafu.

# 10

*Dawuda ya ci Ammonawa da yaƙi*
*(1 Tarihi 19.1-19)*

† **8:18** Ko kuwa su ne firistoci

1 Ana nan sai sarkin Ammonawa ya rasu, ɗansa Hanun kuwa ya gāje shi a matsayin
sarki. 2 Dawuda ya yi tunani a ransa ya ce, “Zan yi wa Hanun ɗan Nahash alheri
kamar yadda mahaifinsa ya yi mini.” Saboda haka sai Dawuda ya aiki jakadu su yi
masa ta’aziyyar mutuwar mahaifinsa.

Sa’ad da mutanen Dawuda suka isa ƙasar Ammonawa, 3 sai manyan mutanen
Ammonawa suka ce wa Hanun shugabansu, “Kana tsammani Dawuda yana girmama
mahaifinka ne da ya aiko da jakadu su kawo maka ta’aziyya? Ai, wayo ya yi don yǎ
ga asirin birninmu, yǎ san ƙarfinmu, yǎ kuma ci mu da yaƙi.” 4 Saboda haka Hanun
ya kama mutanen Dawuda ya aske rabin gemun kowannensu, ya yayyage rigunarsu
daidai ɗuwawu, sa’an nan ya sallame su.

5 Sa’ad da aka gaya wa Dawuda game da wannan, sai ya aiki manzanni su taryi
waɗannan mutanen da aka ci mutuncinsu, gama an wulaƙanta su ƙwarai. Sai sarki
ya ce musu, “Ku dakata a Yeriko har sai gemunku ya sāke girma, sa’an nan ku dawo.”

6 Da Ammonawa suka gane cewa Dawuda ya ji fushi da su sosai saboda abin da
suka yi, sai suka yi hayar sojojin ƙasar Arameyawa dubu ashirin daga Bet Rehob da
Aram-Zoba, suka kuma yi hayar sarkin Ma’aka tare da mutum dubu ɗaya, suka kuma
yi hayar maza dubu goma sha biyu daga Tob.

7 Da jin haka, Dawuda ya tura Yowab da dukan sojojin yaƙi. 8 Ammonawa suka
fita suka ja dāgār yaƙi a ƙofar shiga birninsu, yayinda Aram-Zoba, da na Rehob, da
mutane Tob, da kuma na Ma’aka, suka ja tasu dāgār a karkara.

9 Yowab ya ga cewa an ja masa dāgār yaƙi gaba da baya; saboda haka sai ya zaɓi
waɗansu shahararrun sojoji cikin Isra’ila, ya sa su gabza da Arameyawa. 10 Ya sa
sauran mutanen a ƙarƙashin Abishai ɗan’uwansa, ya sa su gabza da Ammonawa.
11 Yowab ya ce, “In Arameyawa suka fi ƙarfina, sai ku kawo mini gudummawa; amma
in Ammonawa suka fi ƙarfinku, sai mu kawo muku gudummawa. 12 Ku yi ƙarfin hali,
mu kuma yi yaƙi da ƙarfin zuciya saboda mutanenmu da kuma birane Allahnmu.
UBANGIJI zai yi abin da yake da kyau a idanunsa.”

13 Sa’an nan Yowab da rundunar da take tare da shi suka ci gaba don su gabza
da Arameyawa, Arameyawa kuwa suka gudu a gabansa. 14 Da Ammonawa suka ga
Arameyawa suna gudu, sai su ma suka ruga da gudu a gaban Abishai, suka shiga
cikin birni. Sa’an nan Yowab ya komo Urushalima daga wurin yaƙin da ya yi da
Ammonawa.

15 Bayan Arameyawa suka ga Isra’ila ta ci su da yaƙi, sai suka sāke tattara kansu.
16 Hadadezer sarkin Zoba ya aika a kawo Arameyawan da suke ƙetaren Kogin
Yuferites. Suka iso Helam a ƙarƙashin shugabancin Shobak, shugaban dukan sojojin
Hadadezer.

17 Da aka gaya wa Dawuda wannan, sai ya tattara dukan Isra’ila, ya ƙetare Urdun,
ya je Helam. Arameyawa suka ja dāgār yaƙinsu, suka kara da Dawuda. 18 Amma
Arameyawa suka gudu a gaban Isra’ila, Dawuda kuwa ya kashe mahayan keken
yaƙinsu ɗari bakwai, da sojojin ƙasa dubu arba’in. Ya bugi Shobak, shugaban
ƙungiyar sojansu ya kuwa mutu a can. 19 Sa’ad da dukan sarakuna waɗanda suke
abokan tarayya na Hadadezer suka ga Isra’ila sun ci su da yaƙi, sai suka yi sulhu da
Isra’ilawa, suka kuma zama bayinsu.

Wannan ya sa Arameyawa suka ji tsoron ƙara kai wa Ammonawa gudummawa.

# 11

*Dawuda da Batsheba*
*(1 Tarihi 20.1)*

1 Da bazara, a lokacin da sarakuna sukan fita zuwa yaƙi, sai Dawuda ya aiki Yowab
tare da mutanen sarki, da dukan Isra'ila. Suka je suka hallaka Ammonawa, suka
kuma yi wa Rabba kwanton ɓauna. Amma Dawuda ya yi zamansa a Urushalima.
2 Wata rana da yamma, Dawuda ya tashi daga gadonsa, ya zaga kewaye a rufin
fadansa. Daga rufin ya ga wata mace tana wanka. Matar kyakkyawa ce ƙwarai. 3 Sai
Dawuda ya aiki wani yă bincika ko wace ce ita, sai mutumin ya dawo ya ce, "Wannan
ba Batsheba ba ce, 'yar Eliyam matar Uriya, mutumin Hitti?" 4 Sa'an nan Dawuda ya
aiki manzanni su kawo masa ita. Ta zo wurinsa shi kuma ya kwana da ita (A lokacin
kuwa ta gama tsarkake kanta ke nan daga jinin haila.) Sa'an nan[*] ta tafi gida. 5 Matar
ta yi ciki, ta kuwa aika wa Dawuda, tana cewa, "Ina da ciki."
6 Saboda haka Dawuda ya aika saƙo wa Yowab ya ce, "Ka aiko mini da Uriya
mutumin Hitti." Yowab kuwa ya aika da shi wajen Dawuda. 7 Da Uriya ya zo wurinsa,
sai Dawuda ya tambaye shi lafiyar Yowab da sojojin, da kuma yaya yaƙin yake tafiya.
8 Sa'an nan Dawuda ya ce wa Uriya, "Gangara gidanka ka wanke ƙafafunka." Saboda
haka Uriya ya bar fadar, sarki kuma ya aika masa da kyauta. 9 Amma Uriya ya kwanta
a ƙofar fada tare da dukan bayin maigidansa, bai kuwa tafi gidansa ba.
10 Da aka gaya wa Dawuda, "Uriya bai tafi gida ba," sai Dawuda ya tambaye shi ya
ce, "Ba ka zo daga wuri mai nisa ba? Me ya sa ba ka je gida ba?"
11 Sai Uriya ya ce wa Dawuda, "Akwatin Alkawari, da Isra'ila, da Yahuda suna zama
cikin tentuna, kuma maigidana Yowab da mutanen ranka yă daɗe suna a sansani a
fili. Yaya zan je gidana in ci in sha in kuma kwana da matata? Muddin kana a raye,
ba zan yi irin wannan abu ba!"
12 Sai Dawuda ya ce masa, "Ka ƙara dakata a nan kwana ɗaya, gobe kuwa in sallame
ka." Saboda haka Uriya ya dakata a Urushalima a ranar, da kuma ta biye. 13 Dawuda
ya gayyace shi, ya kuwa ci ya sha tare da shi, Dawuda ya sa ya bugu tilis. Amma
da yamma Uriya ya koma ya kwanta a tabarmarsa cikin bayin maigidan sarki; bai je
gida ba.
14 Da safe Dawuda ya rubuta wa Yowab wasiƙa ya ba wa Uriya. 15 A ciki wasiƙar
ya rubuta, "Tura Uriya a gaba inda yaƙi ya fi zafi. Sa'an nan ka janye daga gare shi
don a buge shi yă mutu."
16 Saboda haka yayinda Yowab ya kai yaƙi kusa da birnin, sai tura Uriya a inda ya
sani akwai jarumawan Ammon na gaske. 17 Sa'ad da mutanen garin suka fito suka
yaƙi Yowab, sai waɗansu mutane daga sojojin Dawuda suka mutu; Uriya mutumin
Hitti ma ya mutu.
18 Yowab ya aika wa Dawuda cikakken labari batun yaƙin. 19 Ya umarci manzon
ya ce, "Da ka gama yin wa sarki wannan batun yaƙin, 20 wataƙila sarki yă husata,
yă tambaye ka, 'Me ya sa kuka je kusa da birnin don ku yi yaƙi? Ba ku san cewa za
su yi harbi daga katanga ba? 21 Wane ne ya kashe Abimelek ɗan Yerub-Beshet?[†] Ba
mace ce ta jefa dutsen niƙa a kansa daga katanga, ta haka ya mutu a Tebez ba? Me
ya sa kuka je kurkusa da katangar?' In ya tambaye ka wannan, sai ka ce masa, 'Har
bawanka Uriya mutumin Hitti ma ya mutu.' "
22 Manzon ya tashi ya tafi, da ya iso kuwa sai ya gaya wa Dawuda dukan abin da
Yowab ya aike shi yă faɗa. 23 Manzon ya ce wa Dawuda, "Mutanen sun sha kanmu
suka fito suka yaƙe mu a fili, amma muka kore su har ƙofar birni. 24 Sa'an nan
maharba suka yi ta harbi daga katanga har waɗansu mutanen sarki suka mutu. Ban
da haka ma, Uriya mutumin Hitti bawan sarki ya mutu."

[*] **11:4** Ko kuwa da ita. Sa'ad da ta tsarkake kanta daga al'adarta [†] **11:21** An kuma san shi kamar Yerub-Ba'al (wato, Gideyon).

[25] Dawuda ya ce wa manzon, "Ka gaya wa Yowab, 'Kada ka bar wannan yă dame
ka; yadda takobi ya lamushe wannan, haka zai lamushe wancan ma. Ku ƙara matsa
wa garin lamba, ku hallaka shi.' Ka faɗa haka don ka ƙarfafa Yowab."
[26] Da matar Uriya ta ji cewa mijinta ya mutu, sai ta yi makoki saboda shi. [27] Bayan
kwanakin makoki suka ƙare, Dawuda ya sa aka kawo ta gidansa, ta kuwa zama
matarsa, ta kuma haifa masa ɗa. Sai dai abin da Dawuda ya yi bai gamshi Ubangiji
ba.

# 12

*Natan ya tsawata wa Dawuda*

[1] Ubangiji ya aiki Natan wurin Dawuda. Da ya tafi wajensa, sai ya ce, "An yi
waɗansu mutum biyu a wani gari, ɗaya mai arziki, ɗayan kuma matalauci. [2] Mai
arzikin yana da babban garken tumaki, da kuma shanu, [3] amma matalauci ba shi
da kome sai 'yar tunkiyar da ya sayo. Ya yi kiwonta, ta kuwa yi girma tare shi da
yaransa. Takan ci tare da shi ta sha ruwa a kwaf nasa, har ma ta kwanta a ƙirjinsa.
Ta ma zama kamar 'ya a gare shi.
[4] "To, sai ga wani baƙo ya zo wurin mai arzikin nan, amma mai arzikin ya ƙi yă
kama tunkiyarsa, ko saniyarsa yă yanka don yă shirya wa baƙon da ya zo abinci. A
maimako, sai ya je ya kama 'yar tunkiyan nan ta matalaucin ya yanka ya shirya wa
mutumin da ya zo masa."
[5] Dawuda ya husata ƙwarai da mutumin, ya ce wa Natan, "Muddin Ubangiji yana a
raye, mutumin da ya yi wannan ya cancanci yă mutu! [6] Dole yă biya diyyar tunkiyan
nan sau huɗu, domin ya aikata haka ba tausayi."
[7] Sai Natan ya ce wa Dawuda, "Kai ne mutumin! Ga abin da Ubangiji, Allah ya ce,
'Na naɗa ka sarki bisa Isra'ila, na kuma cece ka daga hannun Shawulu. [8] Na ba ka
gidan maigidanka, da matan maigidanka duka. Na ba ka gidan Isra'ila da Yahuda.
Da a ce dukan waɗannan sun kāsa maka, ai, da na ƙara maka. [9] Me ya sa ka rena
maganar Ubangiji ta wurin yin mugunta haka a idonsa? Ka kashe Uriya mutumin
Hitti da takobi, ka kuma ɗauki matarsa tă zama matarka. Ka kashe shi da takobin
Ammonawa. [10] To, fa, takobi ba zai taɓa rabu da gidanka ba, domin ka rena ni, ka
kuma ƙwace matar Uriya mutumin Hitti ta zama matarka.'
[11] "Ga abin da Ubangiji yana cewa, 'Daga cikin iyalinka zan kawo masifa a kanka.
A idanunka zan ɗauki matanka in ba wa wani da yake kusa da kai, zai kuwa kwana
da su da rana tsaka. [12] Ka aikata wannan a ɓoye, amma zan aikata wannan da rana
tsaka, a gaban dukan Isra'ila.' "
[13] Sai Dawuda ya ce wa Natan, "Na yi wa Ubangiji zunubi."
Natan ya ce, "Ubangiji ya yafe maka zunubin. Ba za ka mutu ba. [14] Amma saboda
ka yi haka ka sa abokan gāba suka rena Ubangiji,* yaron da aka haifa maka zai
mutu."
[15] Bayan Natan ya tafi gida, sai Ubangiji ya bugi yaron da matar Uriya ta haifa
wa Dawuda, ya kuwa kamu da ciwo. [16] Dawuda ya roƙi Allah saboda yaron. Ya yi
azumi, ya kuma shiga gidansa ya kwana kwance a ƙasa. [17] Dattawan iyalinsa suka
tsaya kusa da shi don su ɗaga shi daga ƙasa, amma ya ƙi, bai kuwa ci wani abu tare
da su ba.
[18] A rana ta bakwai sai yaron ya rasu. Barorin Dawuda suka ji tsoro su gaya masa
cewa yaron ya mutu, gama sun yi tunani cewa, "Yayinda yaron yake da rai, mun yi
magana da Dawuda bai ji mu ba. Yaya za mu gaya masa yaron ya mutu? Ai, zai yi
wa kansa ɓarna."

* **12:14** Nassin Masoretik; wani daɗaɗɗen naɗaɗɗen littafin al'adar Ibraniyanci yana da wannan ka nuna cikakken reni wa Ubangiji.

19 Dawuda ya gane bayinsa suna wa juna raɗan wani abu, sai ya gane yaron ya
mutu. Sai ya ce, "Yaron ya rasu ko?"
Suka ce, "I, ya rasu."
20 Sa'an nan Dawuda ya tashi daga ƙasa. Bayan ya yi wanka, ya shafa mai, ya
kuma canja rigunarsa, sa'an nan ya shiga gidan UBANGIJI ya yi sujada. Sai ya tafi
gidansa, ya nemi a ba shi abinci, aka ba shi, ya kuwa ci.
21 Barorinsa suka ce masa, "Me ya sa kake yin haka? Yayinda yaron yake da rai,
ka yi azumi, ka kuma yi kuka, amma yanzu da yaron ya mutu, ka tashi, ka kuma ci
abinci!"
22 Ya ce musu, "Yayinda yaron yake da rai, na yi azumi, na kuma yi kuka. Na yi
tunani na ce, 'Wa ya sani? Ko UBANGIJI zai yi mini alheri yă bar yaron yă rayu.'
23 Amma yanzu da ya mutu, me zai sa in yi azumi? Zan iya dawo da shi ne? Ni zan
je wajensa, ba shi zai dawo wurina ba."
24 Sai Dawuda ya yi wa matarsa Batsheba ta'aziyya, ya kuma tafi wurinta ya kwana
da ita. Ta kuma haifi ɗa, suka ba shi suna Solomon. UBANGIJI ya ƙaunace shi; 25 kuma
saboda UBANGIJI ya ƙaunace shi, sai ya aika da saƙo ta wurin annabi Natan yă ba shi
suna Yedidiya.†

*(1 Tarihi 20.1-3)*

26 Ana cikin haka, sai Yowab ya yi yaƙi da Rabba na Ammonawa, ya kuma ƙwace
babban birnin. 27 Sa'an nan Yowab ya aika manzanni wurin Dawuda yana cewa,
"Na yaƙi Rabba na kuma ƙwace hanyar samun ruwanta. 28 Yanzu fa ka tattara saura
rundunoni ka fāɗa wa birnin ka ci shi. In ba haka ba zan karɓe birnin, a kuma kira
shi da sunana."
29 Saboda haka Dawuda ya tattara sauran rundunar sojojin suka tafi Rabba suka
fāɗa masa suka kuma ci shi. 30 Ya ɗauke rawanin daga kan sarkinsu,‡ nauyinsa ya
kai talenti§, na zinariya, an kuma yi masa ado da duwatsu masu daraja, aka aza shi
a kan Dawuda. Ya kuma kwashe ganima mai yawa daga garin. 31 Ya fito da mutanen
da suke a can, ya sa su su yi aiki da zarto, da diga, da kuma gatari, ya kuma sa su
bugan bulok. Haka ya yi wa dukan garuruwan Ammonawa. Sa'an nan Dawuda da
dukan sojoji suka koma Urushalima.

# 13

*Amnon da Tamar*

1 Ana nan sai Amnon ɗan Dawuda ya fara son Tamar, kyakkyawar 'yar'uwar
Absalom ɗan Dawuda.
2 Amnon ya matsu ƙwarai har abin ya sa shi ciwo saboda ƙanuwarsa Tamar. Ya
gane zai zama da wuya yă sadu da Tamar ita kaɗai, gama ba ta taɓa kwana da namiji
ba.
3 To, Amnon yana da wani aboki mai suna Yonadab, ɗan Shimeya, ɗan'uwan
Dawuda. Yonadab dai mai wayo ne ƙwarai. 4 Ya tambayi Amnon ya ce, "Don me
kowace safiya fuskarka a ɓace take? Kai ba yaron sarki ba ne? Faɗa mini, me ke
faruwa?"
Amnon ya ce masa, "Ina son Tamar ƙanuwar wan nawa Absalom ne."
5 Yonadab ya ce, "Je gado ka kwanta kamar ba ka da lafiya. Sa'ad da mahaifinka
ya zo ganinka, sai ka ce masa, 'Ina so ƙanuwata Tamar tă kawo mini wani abu in ci.
Bari tă shirya abincin a gabana don in ganta, in kuma ci daga hannunta.' "
6 Sai Amnon ya kwanta sai ka ce yana ciwo. Da sarki ya zo don ganinsa, sai Amnon
ya ce, "Zan so ƙanuwata Tamar tă zo tă shirya mini abinci a gabana, don in ci daga
hannunta."

† **12:25** Yedidiya yana nufin ƙaunace na UBANGIJI. ‡ **12:30** Ko kuwa na Milkom (wato, Molek). § **12:30** Wato, wajen fam 75 (wajen kilo 34)

7 Dawuda kuwa ya aika wa Tamar a fada, ya ce, "Ki je gidan Amnon ɗan'uwanki,
ki yi masa abinci." 8 Saboda haka Tamar ta tafi gidan ɗan'uwanta Amnon, wanda
yake kwance. Ta ɗauki fulawa, ta kwaɓa, ta yi burodi a gabansa ta toya shi. 9 Sa'an
nan ta juye a kasko ta ba shi burodin, amma ya ƙi ci.
Amnon ya ce, "A sa kowa yă fita daga nan." Saboda haka kowa ya fita ya bar shi.
10 Sa'an nan Amnon ya ce wa Tamar, "Kawo abincin a nan a cikin ɗakin kwanciyata,
don in ci daga hannunki." Tamar kuwa ta ɗauki burodin da ta toya, ta kawo wa
ɗan'uwanta Amnon a ciki ɗakin kwanciyarsa. 11 Amma da ta kai masa don yă ci, sai
ya cafke ta ya ce, "Zo in kwana da ke, 'yar'uwata."
12 Ta ce, "Kada ka yi wannan ɗan'uwana! Kada ka tilasta ni. Bai kamata a yi
irin wannan abu a Isra'ila ba! Kada ka yi wannan mugun abu. 13 Ni fa, ina zan sa
kaina saboda kunya? Kai kuma za ka zama kamar wani mugun wawa a Isra'ila. Ina
roƙonka ka yi wa sarki magana; ba zai hana ni aurenka ba." 14 Amma Amnon ya ƙi
yă saurare ta, da yake ya fi ta ƙarfi, sai ya yi mata fyaɗe.
15 Bayan ya yi lalata da ita sai Amnon ya ƙi ta da mummunan ƙiyayya. Zahiri ya
ƙi ta fiye da ya ƙaunace ta. Sai Amnon ya ce mata, "Tashi, ki fita!"
16 Ta ce, "A'a! Korina zai fi muni da abin da ka riga ka yi mini."
Amma ya ƙi yă saurare ta. 17 Sai ya kira bawansa ya ce, "Fitar da matan nan daga
nan, ka rufe ƙofa." 18 Saboda haka bawansa ya fitar da ita, ya kuma sa aka rufe
ƙofa. Tana sanye da doguwar riga mai kayan ado masu tsada,* gama wannan ne
irin kayan da budurwai 'ya'yan sarki mata suke sawa. 19 Sai Tamar ta zuba toka a
kanta, ta kuma yayyage doguwar riga mai kayan adon† da take sanye da shi. Ta sa
hannunta a kai, ta tafi tana kuka da ƙarfi.
20 Absalom ɗan'uwanta ya ce mata, "Amnon, ɗan'uwanki ya ɓata ki ko? To, ki yi
shiru 'yar'uwata; ai, ɗan'uwanki ne. Kada wannan abu yă dame ki." Tamar kuwa
ta zauna a gidan ɗan'uwanta Absalom, zaman kaɗaici.
21 Da Sarki Dawuda ya ji dukan abin da ya faru, sai ya husata ƙwarai. 22 Absalom
kuwa bai yi wa Amnon wata magana ta alheri ko ta mugunta ba; ya ƙi jinin Amnon
domin ya ci mutuncin ƙanuwarsa Tamar.

### *Absalom ya kashe Amnon*

23 Bayan shekaru biyu, sa'ad da masu askin tumakin Absalom suna Ba'al-Hazor,
kusa da iyakar Efraim, sai ya gayyaci dukan 'ya'yan sarki maza a can. 24 Sai Absalom
ya je wurin sarki ya ce, "Bawanka ya sa masu askin tumaki sun zo. Ko sarki da
fadawansa za su zo tare da ni?"
25 Sarki ya ce, "A'a ɗana, bai kamata dukanmu mu tafi ba; don kada nauyi yă yi
maka yawa." Absalom dai ya dāge, duk da haka sarki ya ƙi yă je, sai dai ya albarkace
shi.
26 Sa'an nan Absalom ya ce, to, "In ba za ka ba, ina roƙonka bari Amnon ɗan'uwana
yă zo tare da mu."
Sarki ya ce masa, "Don me zai tafi tare da kai?" 27 Amma Absalom ya nace don
sarki yă yarda, saboda haka sarki ya bar Amnon da sauran 'ya'yan sarki maza su tafi
tare da shi.
28 Absalom ya umarci mutanensa ya ce, "Ku saurara! Sa'ad da Amnon ya bugu
sosai da giya na kuma ce muku, 'Ku bugi Amnon,' sai ku kashe shi. Kada ku ji tsoro.
Ashe, ba ni ne na ba ku wannan umarni ba? Ku yi ƙarfin hali, ku kuma yi jaruntaka."
29 Saboda haka mutanen Absalom suka yi wa Amnon abin da Absalom ya umarta.
Sai dukan sauran 'ya'yan sarki maza suka hau dawakansu suka gudu.

---

* **13:18** Ba a tabbatar da ma'anar kalman nan a Ibraniyanci ba. † **13:19** Ba a tabbatar da kalmar Ibraniyancin nan ba.

30 Yayinda suke kan hanyarsu, sai labari ya kai kunnen Dawuda cewa, "Absalom
ya kashe dukan 'ya'yan sarki maza; ko ɗayansu Absalom bai rage ba." 31 Sai sarki
ya tashi, ya yage tufafinsa, ya kuma kwanta a ƙasa; dukan bayinsa kuwa suka tsaya
da rigunansu yagaggu.
32 Amma Yonadab, ɗan Shimeya ɗan'uwan Dawuda ya ce, "Kada ranka yă daɗe
yă yi tunani cewa an kashe dukan 'ya'yan sarki maza; Amnon ne kaɗai ya mutu.
Wannan ce niyyar Absalom tun lokacin da Amnon ya yi wa Tamar 'yar'uwansa fyaɗe.
33 Kada mai girma sarki yă damu da jita-jitan nan cewa an kashe dukan 'ya'yan sarki
maza. Amnon ne kaɗai ya mutu."
34 Ana cikin haka, sai Absalom ya gudu.
To, mutumin da yake tsaro a wannan lokaci ya ɗaga kai sai ya ga mutane da yawa
a hanya, yamma da shi, suna gangarowa daga gefen tudu. Sai mai tsaron ya je ya
gaya wa sarki cewa, "Na ga mutane ta wajen Horonayim, a gefen tudu."‡
35 Yonadab ya ce wa Sarki, "Duba, ga 'ya'yan sarki maza sun zo; ya faru kamar dai
yadda bawanka ya faɗa."
36 Yana gama magana, sai ga 'ya'yan sarki maza suka shigo suna kuka da ƙarfi.
Sarki ma da dukan bayinsa suka yi kuka mai zafi.
37 Absalom ya gudu ya tafi wurin Talmai ɗan Ammihud, sarkin Geshur. Amma
Sarki Dawuda ya yi ta makokin ɗansa kowace rana.
38 Bayan Absalom ya gudu sai ya je wurin Geshur, ya zauna a can shekara uku.
39 Sai zuciyar sarki Dawuda ya komo kan Absalom, gama an yi masa ta'aziyya game
da mutuwar Amnon.

# 14

*Absalom ya koma Urushalima*

1 Yowab, ɗan Zeruhiya ya gane cewa zuriyar sarki ta koma ga Absalom. 2 Saboda
haka Yowab ya aiki wani zuwa Tekowa, ya sa a zo da wata mace mai hikima. Ya ce
mata, "Ki yi kamar kina makoki. Ki sa rigar makoki, kada kuwa ki shafa mai. Ki yi
kamar macen da ta yi kwanaki da yawa, tana makokin matattu. 3 Sa'an nan ki je
wurin sarki, ki ce masa haka." Sai Yowab ya faɗa mata duk abin da za tă faɗa.
4 Da macen da ta fito daga Tekowa ta je wajen sarki, sai ta rusuna har ƙasa don
bangirma, sai ta ce, "Ka taimake ni, ya sarki!"
5 Sarki ya ce mata, "Mece ce matsalarki?"
Sai ta ce, "Tabbatacce, ni gwauruwa ce; mijina ya mutu. 6 Baiwarka tana da 'ya'ya
maza biyu. Suka yi faɗa da juna a fili, kuma ba wanda yake can don yă raba su.
Ɗayan ya bugi ɗayan, ya kashe shi. 7 To, ga duk iyali sun hau kan baiwarka, suna
cewa, 'Ki ba mu ɗayan da ya kashe ɗan'uwansa mu kashe don ran ɗan'uwansa da
ya kashe; sa'an nan za mu hallaka magājin shi ma.' Za su kashe garwashin wuta mai
ci da nake da shi kaɗai, su bar mijina ba suna, ba jika, a duniya."
8 Sarki ya ce wa macen, "Koma gida, zan ba da umarni a madadinki."
9 Amma macen da ta fito daga Tekowa ta ce, "Ranka yă daɗe, sarki! Bari alhakin
shari'arka yă kasance a kaina da gidan mahaifina, kai sarki da gidan mulkinka, ba
ku da laifi a ciki."
10 Sai sarki ya ce, "In wani ya yi miki magana, ki kawo shi wurina, ba zai kuwa
ƙara damunki ba."
11 Sai ta ce, "To, bari sarki yă rantse da UBANGIJI Allahnsa don yă hana mai ramako
yin ƙarin hallakawar da aka yi, domin kada a hallaka ɗana."
Sai ya ce, "Muddin UBANGIJI yana a raye, babu gashi guda na ɗanki da zai fāɗi
ƙasa."

‡ **13:34** Seftuwajin; Ibraniyanci ba su da wannan jumli.

12 Sai matar ta ce, "Bari baiwarka ta ƙara yin magana sau ɗayan nan wa ranka yă
daɗe."

Ya ce, "Ki faɗa."

13 Matar ta ce, "To, don me ka yi wa mutanen Allah irin wannan abu? Sa'ad da sarki
ya ce haka, ashe, ba ka hukunta kanka ke nan ba, tun da yake sarki bai yarda ɗansa
yă komo gida ba? 14 Kamar ruwan da ya zuba a ƙasa, wanda ba a iya kwasa, haka
dole mu mutu. Amma Allah ba ya ɗaukan rai; a maimako, yakan ƙirƙiro hanyoyi
domin mutumin da aka kora kada yă kasance yasasshe daga gare shi.

15 "Yanzu ga shi na zo don in faɗa wannan wa ranka yă daɗe sarki, don mutane
sun tsorata ni. Baiwarka ta yi tunani ta ce, 'Zan yi magana wa sarki; wataƙila yă yi
abin da baiwarsa ta roƙa. 16 Wataƙila sarki zai yarda yă ceci baiwarsa daga hannun
mutumin nan da yake ƙoƙari yă hallaka ni da ɗana daga gādon da Allah ya ba mu.'

17 "Yanzu kuwa baiwarka tana cewa, 'Bari magana ranka yă daɗe sarki yă ba ni
hutu, gama ranka yă daɗe sarki yana kama da mala'ikan Allah cikin rarrabe nagarta
da mugunta. Bari UBANGIJI Allahnka yă kasance tare da kai.' "

18 Sai sarki ya ce wa matar, "Kada ki ɓoye mini kome daga abin da zan tambaye
ki."

Matar ta ce, "Bari ranka yă daɗe sarki yă yi tambaya."

19 Sarki ya ce, "Anya, babu hannun Yowab a cikin dukan wannan?"

Matar ta ce, "Muddin kana a raye, ranka yă daɗe sarki, ba wanda zai juya dama ko
hagu daga wani abin da ranka yă daɗe sarki ya faɗa. I, bawanka Yowab ne ya umarce
ni in yi wannan, shi ne kuma ya sa kalmomin nan a bakin baiwarka. 20 Bawanka
Yowab ne ya yi haka don yă daidaita al'amura. Ranka yă daɗe yana da hikima iri ta
mala'ikan Allah, ya san dukan kome da yake faruwa a ƙasar."

21 Sarki ya ce wa Yowab, "To, da kyau, zan yi haka. Je ka, ka dawo da saurayin nan
Absalom."

22 Yowab ya rusuna har ƙasa don bangirma, ya kuma yi wa sarki kyakkyawar fata.
Yowab ya ce, "Yau, bawanka ya sani ya sami tagomashi a gare ka, ranka yă daɗe
sarki, gama sarki ya ji roƙon bawansa."

23 Sa'an nan Yowab ya tafi Geshur ya dawo da Absalom Urushalima. 24 Amma sarki
ya ce, "Yă tafi gidansa; kada yă zo yă gan ni." Saboda haka Absalom ya tafi gidansa,
bai kuwa je ganin sarki ba.

25 A cikin dukan Isra'ila babu wanda ake yabon kyansa kamar Absalom. Tun daga
kansa har zuwa tafin ƙafansa babu tabo a jikinsa. 26 A duk sa'ad da ya aske gashin
kansa (yakan aske kansa lokaci-lokaci sa'ad da ya yi masa nauyi) yakan auna shi,
nauyin gashin kuwa yakan kai wajen shekel ɗari biyu a ma'aunin da ake awo.

27 Aka haifa wa Absalom 'ya'ya uku maza da 'ya mace guda. Sunanta Tamar, ta
kuwa zama kyakkyawan mace ƙwarai.

28 Absalom ya zauna a Urushalima shekara biyu amma ba tare da ganin fuskar
sarki ba. 29 Sai Absalom ya aika a kira masa Yowab don yă aike shi wurin sarki,
amma Yowab ya ƙi zuwa. Saboda haka ya sāke aika sau na biyu, amma ya ƙi yă zo.
30 Sai ya ce wa bayinsa, "Duba, gonar Yowab tana gab da tawa, kuma yana da sha'ir
a can. Ku je ku sa mata wuta." Sai bayin Absalom suka sa wa gonar wuta.

31 Sa'an nan Yowab ya tafi gidan Absalom ya ce masa, "Me ya sa bayinka suka sa
wa gonata wuta?"

32 Absalom ya ce wa Yowab, "Kai, na aika, 'Ka zo nan don in aike ka wurin sarki ka
tambaya, "Me ya sa na dawo daga Geshur? Ai, ya fi mini a ce ina can har yanzu!" '
Yanzu kuwa, ina so in ga sarki, kuma idan na yi wani laifi, to, yă kashe ni."

[33] Saboda haka Yowab ya tafi wurin sarki ya gaya masa wannan. Sai sarki ya aika
aka zo da Absalom, ya kuma rusuna da fuskarsa har ƙasa a gaban sarki. Sarki kuwa
ya sumbaci Absalom.

# 15

*Absalom ya shirya maƙarƙashiya*

[1] Ana nan sai Absalom ya samo wa kansa wata keken yaƙi da dawakai tare da
mutum hamsin da za su sha gabansa. [2] Absalom yakan tashi da sassafe yă tsaya a
gefen hanyar shigar ƙofar birni. Duk sa'ad da wani ya zo da ƙara don a kai gaban
sarki yă yi shari'a, Absalom yakan kira shi yă ce, "Daga wane gari ka fito?" Sai
mutumin yă amsa yă ce, "Bawanka ya fito a ɗaya daga cikin kabilan Isra'ila." [3] Sai
Absalom yă ce masa, "Ga shi, ƙararka daidai ne, tana kuma da gaskiya, sai dai ba
wakilin sarkin da zai ji ka." [4] Absalom kuwa yakan ƙara da cewa, "Da a ce an naɗa ni
alƙali a ƙasar mana! Da duk mai ƙara, ko kuka wanda zai zo wurina, zan in tabbatar
an yi masa adalci."

[5] Kuma duk sa'ad da wani ya zo wurin Absalom ya rusuna don yă gaishe shi, sai
Absalom yă sa hannunsa yă ta da shi, yă kuma rungume shi. [6] Absalom ya yi ta yin
haka ga dukan Isra'ilawan da suka zo wurin sarki don neman adalci, ta haka kuwa
ya saci zukatan mutanen Isra'ila.

[7] A ƙarshen shekara huɗu,* Absalom ya ce wa sarki, "Bari in tafi Hebron in cika
alkawarin da na yi wa UBANGIJI. [8] Yayinda bawanka yake zama a Geshur, a Aram,
na yi wannan alkawari, na ce, 'In UBANGIJI ya komo da ni Urushalima, zan yi wa
UBANGIJI sujada a Hebron.' "†

[9] Sarki ya ce, "Ka sauka lafiya." Sai ya tafi Hebron.

[10] Sai Absalom ya aiki manzanni a asirce cikin dukan kabilan Isra'ila, ya ce musu su
ce, "Da zarar kuka ji an busa ƙaho, sai ku ce, 'Absalom sarki ne a Hebron.' " [11] Mutum
ɗari biyu daga Urushalima suka raka Absalom. An gayyace su a matsayin baƙi, suka
kuwa tafi cikin rashin sani, ba su san wani abu game da al'amarin ba. [12] Yayinda
Absalom yake miƙa hadaya, ya aika a kira Ahitofel mutumin Gilo, mai ba wa Dawuda
shawara, yă zo daga Gilo garinsa. Ta haka makircin ya ƙara ƙarfi, masu bin Absalom
kuma suka yi ta ƙaruwa.

*Dawuda ya gudu*

[13] Wani manzo ya zo wurin Dawuda ya ce masa, "Zukatan mutanen Isra'ila sun
koma wajen Absalom."

[14] Sai Dawuda ya ce wa dukan fadawansa da suke tare da shi a Urushalima, "Ku
zo! Mu gudu, in ba haka ba, babu wanda zai tsira daga hannun Absalom. Dole mu
bar nan, nan da nan, in ba haka ba zai tashi da sauri yă fāɗa mana, yă kuma hallaka
garin da takobi."

[15] Sai fadawan sarki suka ce masa, "Barorinka suna a shirye su yi duk abin da
ranka yă daɗe, ya zaɓa."

[16] Sarki ya kama hanya, dukan gidansa kuwa suna biye da shi; amma ya bar
ƙwarƙwarai goma su lura da fada. [17] Ta haka sarki ya kama hanya da dukan mutane
suna biye da shi, suka yi sansani a wani wuri mai ɗan nisa da Urushalima. [18] Dukan
mutanensa suka wuce gabansa, tare da dukan Keretawa da Feletiyawa; da dukan
mutane ɗari shida na Gittiyawan da suka raka shi daga Gat, suka wuce gaban sarki.

[19] Sarki ya ce wa Ittai mutumin Gat, "Don me za ka zo tare da mu? Ka koma ka
zauna tare da Sarki Absalom. Kai baƙo ne, ɗan gudun hijira daga garinka. [20] Jiya-jiya

* **15:7** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na Seftuwajin, Siriyak da Yosefus; Ibraniyanci arba'in † **15:8** Waɗansu
rubuce-rubucen hannu na Seftuwajin; Ibraniyanci ba shi da a Hebron.

ka zo. Yau kuma in sa ka yi ta yawo tare da mu, ga shi ban ma san inda za ni ba?
Koma, ka tafi da 'yan'uwanka. Bari alheri da amincin UBANGIJI su kasance tare da
kai."
21 Amma Ittai ya ce wa sarki, "Muddin UBANGIJI yana a raye kuma muddin ranka
yă daɗe yana a raye, duk inda ranka yă daɗe sarki zai kasance, ko a yi rai ko a mutu,
a can bawanka zai kasance."
22 Dawuda ya ce wa Ittai, "Wuce gaba, taka mu je." Sai Ittai mutumin Gat ya shiga
layi tare da dukan mutanensa da iyalan da suke tare da shi.
23 Dukan ƙauyuka suka yi ta kururuwa yayinda mutanen suke wucewa. Sarki shi
ma ya haye ta Kwarin Kidron, mutane kuma suka ci gaba da tafiya zuwa wajen
hamada.
24 Zadok yana nan tare da su, kuma dukan Lawiyawan da suke tare da shi kuwa
suna ɗauke da akwatin alkawarin Allah. Suka sauke akwatin alkawarin Allah,
Abiyatar ya miƙa hadaya[‡] sai da mutane suka gama fita daga birnin.
25 Sa'an nan sarki ya ce wa Zadok, "Ka komar da akwatin alkawarin Allah cikin
birnin. Idan na sami tagomashi a idon UBANGIJI, zai dawo da ni, yă kuma sa in sāke
gan shi a mazauninsa. 26 Amma in ya ce, 'Ina baƙin ciki da kai,' to, ina a shirye; bari
yă yi abin da ya fi masa."
27 Sarki ya kuma ce wa Zadok firist, "Ashe, kai ba mai duba ba ne? Ka koma
cikin birnin lafiya, tare da ɗanka Ahimawaz, da kuma Yonatan ɗan Abiyatar. Kai da
Abiyatar ku tafi da 'ya'yanku biyu. 28 Zan kuwa jira a mashigai a hamada, sai na
ji daga gare ku." 29 Saboda haka Zadok da Abiyatar suka ɗauki akwatin alkawarin
Allah suka komar da shi Urushalima, suka zauna a can.
30 Amma Dawuda ya ci gaba yana hawan Dutsen Zaitun, yana kuka yayinda yake
tafiya; kansa a rufe, kuma babu takalma a ƙafafunsa. Dukan mutanen da suke tare
da shi suka rufe kawunansu suna ta kuka yayinda suke haurawa. 31 To, an gaya
wa Dawuda cewa, "Ahitofel yana cikin waɗanda suka hadasa maƙarƙashiya tare da
Absalom." Saboda haka Dawuda ya yi addu'a ya ce, "Ya UBANGIJI ka mai da shawarar
Ahitofel ta zama shiririta."
32 Da Dawuda ya isa ƙwanƙoli, inda mutane sun saba yi wa Allah sujada, Hushai,
mutumin Arkitawa kuwa yana can don yă tarye shi, taguwarsa a yage, ga kuma ƙura
a kansa. 33 Sai Dawuda ya ce masa, "In ka tafi tare da ni, za ka zama mini kaya.
34 Amma in ka koma birni, ka gaya wa Absalom, 'Zan zama bawanka, ya sarki; dā
ni bawan mahaifinka ne, amma yanzu zan zama bawanka,' ta haka za ka watsar da
shawarar Ahitofel. 35 Ba Zadok da Abiyatar firistocin nan suna nan tare da kai ba?
Ka gaya musu duk abin da ka ji a fadan sarki. 36 'Ya'yansu biyu maza, Ahimawaz
ɗan Zadok, da kuma Yonatan ɗan Abiyatar, suna can tare da su. Ka aike su wurina
da duk abin da ka ji."
37 Saboda haka Hushai abokin Dawuda ya isa Urushalima yayinda Absalom yake
shigowa birnin.

# 16

*Dawuda da Ziba*

1 Sa'ad da Dawuda ya yi ɗan nesa da ƙwanƙolin, sai ga Ziba mai hidimar
Mefiboshet, yana jira yă tarye shi. Yana da jerin jakuna da sirdi suna ɗauke da
dunƙulen burodi ɗari biyu, da ƙosai busasshen inabi ɗari ɗaya, da kosan 'ya'yan
itace ɓaure guda ɗari, da salka ruwan inabi.
2 Sarki ya ce wa Ziba, "Me ya sa ka kawo waɗannan?"
Ziba ya ce, "Jakuna domin iyalin gidan sarki su hau ne, burodi da 'ya'yan itace
domin mutane su ci, ruwan inabi kuma domin waɗanda suka gaji a hamada."

‡ **15:24** Ko kuwa Abiyatar ya haura

[3] Sai sarki ya ce, "Ina jikar maigidanka?"
Ziba ya ce, "Yana zaune a Urushalima gama yana tsammani cewa, 'Yau gidan Isra'ila za su mayar mini da sarautar kakana.' "
[4] Sai sarki ya ce wa Ziba, "Duk abin da yake na Mefiboshet, ya zama naka."
Ziba ya rusuna ya ce, "Bari in dinga samun tagomashi a gabanka ranka yă daɗe."

*Shimeyi ya la'anci Dawuda*

[5] Yayinda Sarki Dawuda ya kusato Bahurim, sai ga wani mutumin dangin Shawulu
ya fito daga can, sunansa Shimeyi ɗan Gera. Ya fito yana ta la'anta yayinda yake
fitowa. [6] Ya jajjefi Dawuda da dukan fadawan sarki da duwatsu, ko da yake sojoji
da masu gadin sarki na musamman suna kewaye da sarki dama da hagu. [7] Yayinda
yake la'antar, Shimeyi ya ce, "Tafi daga nan, tafi daga nan, mai kisankai, mutumin
banza kawai! [8] UBANGIJI ya kama ka saboda alhakin jinin gidan Shawulu, wanda kake
sarauta a maimakonsa. UBANGIJI ya ba da masarautar ga ɗanka Absalom. Hallaka ta
zo maka domin kai mai kisankai ne!"
[9] Sai Abishai ɗan Zeruhiya ya ce wa sarki, "Ranka yă daɗe, don me wannan mataccen kare yake la'antarka? Bari in je in datse kansa."
[10] Amma sarki ya ce, "Ba ruwana da ku, ku 'ya'yan Zeruhiya. Idan yana la'ana ne domin UBANGIJI ya ce masa, 'La'anci Dawuda,' wa zai ce, 'Don me kake haka?' "
[11] Sa'an nan Dawuda ya ce wa Abishai da dukan fadawansa, "Dana, na cikina, yana
ƙoƙari yă kashe ni. Balle wannan mutumin Benyamin! Ku ƙyale shi, yă yi ta zargi,
UBANGIJI ne ya ce masa yă yi haka. [12] Mai yiwuwa UBANGIJI yă ga azabata, yă sāka
mini da alheri saboda la'anar da nake sha a yau."
[13] Saboda haka Dawuda da mutanensa suka ci gaba da tafiyarsu yayinda Shimeyi
yana tafiya ɗaura da shi a gefen tudu, yana zagi, yana jifansa da duwatsu, yana tayar
masa da ƙura. [14] Sarki da dukan mutanen da suke tare da shi suka isa masauƙinsu
a gajiye. A can fa ya huta.

*Shawarar Hushai da Ahitofel*

[15] Ana cikin haka, Absalom da dukan Isra'ila suka iso Urushalima, Ahitofel kuwa
yana tare da shi. [16] Sai Hushai mutumin Arkitawa, abokin Dawuda ya je wurin
Absalom ya ce masa, "Ran sarki yă daɗe! Ran sarki yă daɗe!"
[17] Absalom ya ce wa Hushai, "Kaunar da kake nuna wa abokinka ke nan? Me ya sa ba ka tafi tare da abokinka ba?"
[18] Hushai ya ce wa Absalom, "A'a, ai, wanda UBANGIJI ya zaɓa ta wurin waɗannan
mutane, da kuma ta wurin dukan mutane Isra'ila, shi zan zama nasa, zan kuma
kasance tare da shi. [19] Ban da haka ma, wane ne zan bauta wa? Ashe, ba ɗan ne zan
bauta wa ba? Kamar dai yadda na bauta wa mahaifinka, haka zan bauta maka."
[20] Absalom ya ce wa Ahitofel, "Ba mu shawararka. Me za mu yi?"
[21] Ahitofel ya ce wa Absalom, "Je ka kwana da ƙwarƙwaran mahaifinka waɗanda
ya bari su lura da fada. Ta haka dukan Isra'ila za su ji cewa ka mai da kanka abin
wari a hancin mahaifinka, dukan hannuwan waɗanda suke tare da kai kuwa za su
sami ƙarfi." [22] Saboda haka suka kafa wa Absalom tenti a bisa rufin ɗaki, a can ya
kwana da ƙwarƙwaran mahaifinsa a gaban dukan Isra'ila.
[23] To, a kwanakin nan shawarar da Ahitofel yakan bayar takan zama kamar wadda aka nemi daga Allah ne. Haka Dawuda da Absalom duk suke ɗaukan dukan shawarar Ahitofel.

## 17

[1] Ahitofel ya ce wa Absalom, "Zan* zaɓi mutum dubu goma sha biyu su fita a daren
nan in fafari Dawuda. [2] Zan fāɗa masa sa'ad da yake cikin gajiya da karayar zuciya.

* **17:1** Ko kuwa Bari in

Zan firgita shi, mutanen da suke tare da shi kuwa za su gudu. Sarki ne kaɗai zan
kashe 3 in dawo da dukan mutanen a gare ka. Mutuwar wanda kake nema zai zama
dawowar duka; dukan mutanen ba za su cutu ba."
4 Wannan shawara ta gamshi Absalom da dukan dattawan Isra'ila.
5 Amma Absalom ya ce, "A kira mini Hushai mutumin Arkitawan nan shi ma, mu
ji abin da zai ce." 6 Da Hushai ya zo wurinsa, sai Absalom ya ce, "Ahitofel ya ba da
wannan shawara. Mu yi abin da ya ce? In ba haka ba, sai ka ba mu ra'ayinka."
7 Hushai ya ce wa Absalom, "Shawarar da Ahitofel ya bayar a wannan lokaci kam,
ba ta da kyau. 8 Ka san mahaifinka da mutanensa mayaƙa ne, suna cikin fushi kamar
mugun beyar da aka ƙwace mata 'ya'ya. Ban da haka ma, mahaifinka gogagge ne a
yaƙi; ba zai kwana da rundunar ba. 9 Kai, ko yanzu ma, ya riga ya ɓuya cikin kogo
ko kuma a wani wuri. In har ya fara kai wa rundunarka hari† duk wanda ya ji, zai
ce, 'An yi kaca-kaca da rundunar da suka bi Absalom.' 10 Kai, ko jarumi mai zuciya
kamar na zaki ma, zai narke don tsoro, gama dukan Isra'ila sun sani mahaifinka
mayaƙi ne, sun kuma san cewa waɗanda suke tare da shi jarumawa ne.
11 "Saboda haka ina ba ka shawara, bari a tara maka dukan Isra'ila, daga Dan zuwa
Beyersheba da yawansu ya yi kamar yashin bakin teku, kai kanka ka jagorance su
zuwa fagen fama. 12 Sa'an nan za mu fāɗa masa duk inda yake, za mu fāɗa masa
kamar yadda raɓa takan fāɗo a bisa ƙasa. Da shi da mutanensa babu ko ɗaya da za
a bari da rai. 13 In ma ya janye zuwa cikin birni, sai dukan Isra'ila su kawo igiyoyi
wa wannan birni, su ja shi zuwa kwari yǎ wargaje, yadda ba za a bar wani dutse a
kan wani ba."
14 Absalom da dukan mutanen Isra'ila suka ce, "Shawarar Hushai mutumin
Arkitawa ta fi ta Ahitofel kyau." Gama UBANGIJI ya ƙudura yǎ wofinta kyakkyawar
shawarar Ahitofel, don yǎ jawo wa Absalom masifa.
15 Hushai ya ce wa Zadok da Abiyatar, firistoci, "Ahitofel ya ba wa Absalom da
dattawan Isra'ila shawara su yi kaza da kaza, amma na ba su shawara su yi haka,
su yi haka. 16 Yanzu sai ku aika wa Dawuda saƙo nan da nan ku ce masa, 'Kada ka
kwana a mashigai cikin hamada; ka tabbata ka haye ba faci, in ba haka ba sarki da
dukan mutanensa za su hallaka.' "
17 Yonatan da Ahimawaz suna zaune a En Rogel. Wata baranya ce za tǎ je ta faɗa
musu, su kuma su tafi su gaya wa Sarki Dawuda don suna tsoro kada a ga suna shiga
birnin. 18 Amma wani saurayi ya gan su, ya gaya wa Absalom. Sai dukansu biyu
suka tashi da sauri suka shiga gidan wani mutum a Bahurim. Yana da rijiya a cikin
gida, sai suka shiga cikinta. 19 Matarsa mutumin kuwa ta kawo tabarma ta shimfiɗa
a bakin rijiyar, sai ta kawo hatsi ta baza a kanta. Ba kuwa wanda ya san abin da ta
yi.
20 Da mutanen Absalom suka zo wurin matan a gidan, suka ce, "Ina Yonatan da
Ahimawaz?"
Matar ta ce, "Tuni, sun haye rafi."‡ Sai mutanen suka yi ta nemansu amma ba su
ga kowa, sai suka koma Urushalima.
21 Bayan mutanen suka tafi, sai su biyun suka fito daga rijiyar suka je suka gaya
wa Sarki Dawuda. Suka ce masa, "Maza ka ƙetare kogi; Ahitofel ya ba wa Absalom
shawara a yi maka kaza da kaza." 22 Saboda haka Dawuda da dukan mutanen da
suke tare da shi suka tashi suka ƙetare Urdun. Kafin wayewar gari, babu wanda ya
rage da bai haye ba.
23 Da Ahitofel ya ga ba a bi shawararsa ba, sai ya hau jakinsa ya koma gidansa a
garinsu. Ya kintsa gidansa sa'an nan ya rataye kansa. Ta haka ya mutu, aka kuma
binne shi a kabarin mahaifinsa.

† **17:9** Ko kuwa Idan waɗansu cikin mutanen suka mutu a harin farko ‡ **17:20** Ko kuwa "Sun wuce ta akulkin tumaki sun nufi wajen ruwa."

24 Dawuda kuwa ya tafi Mahanayim. Absalom kuma ya ƙetare Urdun tare da dukan
mutanen Isra'ila. 25 Absalom ya riga ya naɗa Amasa a kan sojoji a maimakon Yowab.
Amasa kuwa ɗan wani mutum mai suna Itra ne,§ mutumin Ishmayel* wanda ya
auri Abigiyel,† 'yar Nahash, 'yar'uwar Zeruhiya mahaifiyar Yowab. 26 Isra'ilawa da
Absalom suka kafa sansani a ƙasar Gileyad.

27 Sa'ad da Dawuda ya zo Mahanayim, sai Shobi ɗan Nahash daga Rabba ta
Ammonawa, da Makir ɗan Ammiyel daga Lo Debar, da Barzillai mutumin Gileyad
daga Rogelim 28 suka kawo wa Dawuda da mutanensa tabarmai, da kwanoni, da
kayayyakin da aka yi da yumɓu. Suka kuma kawo alkama da sha'ir, da gari, da
soyayyen hatsi, da wake, da waken barewa,‡ 29 da zuma, da kindirmo, da tumaki, da
cukun madarar shanu wa Dawuda da mutanensa su ci. Gama sun ce, "Mutanen suna
jin yunwa, sun kuma gaji, ga ƙishirwa a hamada."

# 18

*Mutuwar Absalom*

1 Dawuda ya tattara mutanen da suke tare da shi, ya naɗa musu komandodi na
dubu-dubu, da na ɗari-ɗari. 2 Dawuda ya sa rundunoni kashi ɗaya bisa uku a
ƙarƙashin Yowab, kashi ɗaya bisa uku a ƙarƙashin Abishai, ɗan'uwan Yowab ɗan
Zeruhiya, kashi ɗaya bisa uku a ƙarƙashin Ittai mutumin Gat. Sai sarki ya ce wa
rundunonin, "Tabbatacce zan tafi tare da ku."

3 Amma mutanen suka ce, "Ba za ka fita ba; gama in ya kasance tilas mu gudu, ba
za su kula da mu ba. Ko da rabinmu sun mutu, ba za su damu ba; amma kai kanka
ka fi mutum dubu goma namu. Zai fi maka ka zauna a cikin gari, ka dinga aika mana
da taimako."

4 Sarki ya ce, "Zan yi duk abin da ya fi muku kyau."

Saboda haka sarki ya tsaya kusa da bakin ƙofa yayinda dukan mutane suke fitowa
a ƙungiyar ɗari-ɗari da ta dubu-dubu. 5 Sarki ya umarci Yowab, Abishai, da Ittai, ya
ce musu, "Ku yi mini hankali da saurayin nan Absalom." Dukan mutane kuwa suka
ji yadda sarki yake ba wa kowane komanda umarni.

6 Rundunonin suka tafi zuwa fili don su yi yaƙi da Isra'ila. Aka kuwa yi yaƙi
a kurmin Efraim. 7 A nan ne mutanen Isra'ila suka sha kashi a hannun mutanen
Dawuda. Waɗanda suka yi rauni da kuma waɗanda suka mutu a ranar sun yi yawa,
mutum dubu ashirin. 8 Yaƙin ya bazu a duk fāɗin ƙauyukan, abin da kurmin ya ci
kawai a ranar ya fi yawan abin da aka kashe da takobi.

9 To, Absalom ya haɗu da mutanen Dawuda. Yana hawan dokinsa, kuma yayinda
dokin ya kusa kai cikin rassan babban itacen oak, sai kan Absalom ya sarƙafe a kan
itacen oak ɗin. Dokin ya wuce da gudu, shi kuwa ya rataye a can yana lilo.

10 Sa'ad da wani daga cikin mutanen ya gan haka, sai ya gaya wa Yowab, "Na ga
Absalom yana rataye a itacen oak."

11 Yowab ya ce wa mutumin da ya ba shi labarin, "Mene! Ka ga shi? Don me ba
ka buge shi har ƙasa nan da nan ba? Ai, da na ba ka shekel goma na azurfa da abin
ɗamarar jarumi."

12 Amma mutumin ya ce wa Yowab, "Ko da za a auna mini azurfa dubu a hannuna,
ba zan miƙa hannuna in taɓa ɗan sarki ba. A kunnuwanmu fa sarki ya umarce ka,

§ **17:25** Da Ibraniyanci Yeter, wani sunan Yeter * **17:25** Ibraniyanci da waɗansu rubuce-rubucen hannu na Seftuwajin; sauran rubuce-rubucen hannu na Seftuwajin (dubi kuma 1Tar 2.17) mutumin Ishmayel Ko kuwa mutumin Yezireyel † **17:25** Da Ibraniyanci Abigiyel, wani sunan Abigiyel. ‡ **17:28** Yawancin rubuce-rubucen hannu na Seftuwajin da Siriyak; Ibraniyanci suna da waken barewa, da soyayyen hatsi ne a nan

da Abishai, da Ittai cewa, 'Ku tsare saurayin nan Absalom a madadina.'* 13 Da na yi
haka da na sa kaina a halin ƙaƙa-ni-ka-yi,† kuma babu abin da zai ɓoyu ga sarki, kai
kuwa za ka janye abinka daga gare ni."

14 Yowab ya ce, "Ba zan ɓata lokaci da kai ba." Saboda haka sai ya ɗauki māsu uku
a hannunsa ya zura su a ƙahon zuciyar Absalom, tun Absalom yana da sauran rai
a maƙale a itacen oak. 15 Masu ɗaukan kayan yaƙin Yowab goma kuwa sun kewaye
Absalom, suka bubbuge shi suka kashe.

16 Sa'an nan Yowab ya busa ƙaho, sai sojoji suka bar fafaran Isra'ila, gama Yowab
ya tsai da su. 17 Suka ɗauki Absalom, suka jefa shi cikin wani babban rami a kurmin,
suka kuwa tula tsibin duwatsu a kansa. Ana cikin haka, sai dukan Isra'ilawa suka
tsere zuwa gidajensu.

18 A lokacin da Absalom yake da rai, Absalom ya gina wa kansa al'amudin tunawa, a
Kwarin Sarki, gama ya yi tunani ya ce, "Ba ni da ɗa namiji wanda zai sa a riƙa tunawa
da ni." Sai ya kira ginshiƙin da sunansa, ana kuwa kira shi Al'amudin Absalom har
wa yau.

### *Dawuda ya yi makoki*

19 Ahimawaz ɗan Zadok ya ce, "Bari in ruga in kai wa sarki labari cewa Ubangiji
ya cece shi daga hannun abokan gābansa."

20 Yowab ya ce, "Ba kai ba ne za ka kai wannan labari a yau ba. Kana iya kai
labarin wani lokaci, amma yau kam ba zai yiwu ba, saboda ɗan sarki ya mutu."

21 Sai Yowab ya ce wa wani mutumin Kush, "Je ka faɗa wa sarki abin da ka gani."
Mutumin Kush ɗin kuwa ya rusuna wa Yowab, sai ya ruga a guje.

22 Ahimawaz ɗan Zadok ya sāke ce wa Yowab, "Ko mene ne zai faru, ina roƙonka
bari in bi bayan mutumin Kush nan."

Amma Yowab ya ce, "Dana me ya sa kake so ka je? Ba ka da labarin da zai jawo
maka lada."

23 Ya ce, "Ko mene ne zai faru, ina so in ruga da gudu."

Sai Yowab ya ce, "Ruga!" Sai Ahimawaz ya sheƙa a guje ya bi ta hanyar fili‡ ya riga
mutumin Kush nan.

24 Yayinda Dawuda yake zaune tsakanin ƙofofin ciki da na waje, sai mai tsaro ya
hau rufin ginin da yake kan hanyar shiga ta wajen katanga. Da ya duba sai ya ga
wani mutum shi kaɗai yana gudu. 25 Mai tsaro ya tā da murya ya faɗa wa sarki.

Sarki ya ce, "In shi kaɗai ne, ya kawo labari mai kyau ke nan." Mutumin ya matso
kusa-kusa.

26 Sai mai tsaron ya ga wani mutum yana zuwa a guje. Sai ya tā da murya ya kira
mai tsaron ƙofa ya ce, "Duba, ga wani mutum kuma yana gudu shi kaɗai!"

Sarki ya ce, "Shi ma yana kawo labari mai daɗi ne."

27 Sai mai tsaron ya ce, "A ganina gudu na farin, ya yi kama da gudun Ahimawaz,
ɗan Zadok."

Sarki ya ce, "Shi mutumin kirki ne, yana zuwa da saƙo mai kyau."

28 Sai Ahimawaz ya tā da murya ya ce wa sarki, "Kome lafiya yake!" Sai ya rusuna
har ƙasa a gaban sarki ya ce, "Yabo ya tabbata ga Ubangiji Allahnka! Ya ba da
mutanen da suka tayar wa ranka yǎ daɗe a hannunsa."

29 Sai sarki ya ce, "Saurayin nan Absalom yana nan da rai?"

Ahimawaz ya ce, "Na ga wani babban rikicewar a daidai lokacin da Yowab yake
gab da aikan bawan sarki da kuma ni, sai dai ban san ko mene ne ba."

30 Sai sarki ya ce, "Koma gefe ka jira a can." Sai ya ja gefe ya tsaya.

---

* **18:12** Kaɗan daga cikin rubuce-rubucen hannu na Ibraniyanci, Seftuwajin, Bulget da Siriyak; za a iya fassara da yawa daga cikin rubuce-rubucen hannu na Ibraniyanci Absalom, ko wane ne kai. † **18:13** Ko kuwa A ce, da na ci amanarsa ‡ **18:23** Wato, filin Urdun

31 Sai ga mutumin Kush ya iso ya ce, “Ranka yă daɗe sarki, ka ji labari mai kyau!
UBANGIJI ya cece ka yau daga dukan waɗanda suka tayar maka.”

32 Sarki ya ce wa mutumin Kush, “Saurayin nan Absalom, yana nan lafiya?”

Mutumin Kush ya ce, “Allah yă sa abokan gāban ranka yă daɗe, da duk waɗanda suka tayar maka da mugunta, su zama kamar saurayin nan.”

33 Sai gaban sarki ya faɗi. Ya haura zuwa ɗakin da yake kan katangar hanyar shiga
ya yi kuka. Yayinda yake tafiya ya ce, “Ya ɗana Absalom! Ɗana, ɗana Absalom! Da
ma a ce ni ne na mutu maimakonka. Ya Absalom, ɗana, ɗana!”

# 19

1 Aka faɗa wa Yowab cewa, “Sarki yana kuka, yana kuma makoki saboda Absalom.”
2 Saboda haka sai nasarar da aka yi a ranar ta zama makoki ga dukan sojoji, gama
a ranar, rundunoni sun ji an ce, “Sarki yana baƙin ciki domin ɗansa.” 3 Mutane fa
suka shiga birni shiru, sai ka ce waɗanda sukan sace jiki don kunya sa'ad da suka
gudo daga yaƙi. 4 Sarki ya rufe fuskarsa ya yi kuka da ƙarfi yana cewa, “Ya ɗana
Absalom! Ya Absalom ɗana, ɗana!”

5 Sai Yowab ya shiga gidan sarki ya ce, “Yau ka kunyatar da dukan mutanenka,
waɗanda ba da daɗewa ba sun ceci ranka, da rayukan 'ya'yanka maza, da na
'ya'yanka mata, da na matanka da kuma na ƙwarƙwaranka. 6 Kana ƙaunar
maƙiyinka, kana ƙin waɗanda suke ƙaunarka. Ka bayyana a fili cewa komandodi da
sojojinsu ba kome ba ne a gare ka. Na ga cewa da za ka yi farin ciki, da a ce Absalom
yana da rai a yau, dukanmu kuma mun mutu. 7 Yanzu ka fita ka ƙarfafa mutanenka.
Na rantse da UBANGIJI, in ba ka fita ba, babu mutum guda da za a bari tare da kai a
daren nan. Wannan zai fi maka muni fiye da kowace irin masifar da ta auko maka
tun ƙuruciyarka har zuwa yanzu.”

8 Saboda haka sarki ya tashi, ya zauna a bakin hanyar shiga. Da aka faɗa wa
mutane cewa, “Sarki yana zaune a bakin hanyar shiga,” sai duk suka zo gabansa.

Ana cikin haka, Isra'ilawa dai sun riga sun tsere zuwa gidajensu.

*Dawuda ya Koma Urushalima*

9 Mutane ko'ina a kabilan Isra'ila, suka yi ta gardama da juna, suna cewa, “Sarki
ne ya cece mu daga hannun abokan gābanmu, shi ne kuma ya kuɓutar da mu daga
hannun Filistiyawa. Amma ga shi ya tsere daga ƙasar saboda Absalom; 10 kuma shi
Absalom, da muka naɗa yă yi mulkinmu, ya mutu a yaƙi. Saboda haka don me ba
kwa ce wani abu game da dawo da sarki?”

11 Sai Sarki Dawuda ya aika da saƙo zuwa wurin Zadok da Abiyatar, firistoci, ya ce,
“Ku tambayi dattawan Yahuda, ‘Me ya sa ku ne za ku zama na ƙarshe a yin tunanin
komar da sarki zuwa fada, da yake abin da ake faɗi ko'ina a Isra'ila ya kai kunnen
sarki a mazauninsa? 12 Ku 'yan'uwana ne, jikina, jinina kuma. To, don me za ku
zama na ƙarshe na yarda a dawo da sarki zuwa fada?’ 13 Ku kuma ce wa Amasa,
‘Ashe, kai ba jikina ba ne da jinina? Allah yă hukunta ni, da hukunci mai tsanani,
idan daga yanzu ba ka zama komandan sojojina a maimakon Yowab ba.’ ”

14 Ta haka ya rinjayi zukatan dukan mutane Yahuda, kamar mutum ɗaya. Suka
aika da saƙo wurin sarki suka ce, “Ka dawo, kai da dukan mutanenka.” 15 Sa'an nan
sarki ya dawo, ya kuma tafi har zuwa Urdun.

To, mutanen Yahuda suka zo Gilgal don su fita su taryi sarki, su kuma kawo shi
ƙetaren Urdun. 16 Shimeyi ɗan Gera, mutumin Benyamin daga Bahurim ya gaggauta,
ya gangara tare da mutanen Yahuda don su taryi Sarki Dawuda. 17 Tare da shi
akwai kabilar Benyamin mutum dubu, tare da Ziba, mai hidimar gidan Shawulu,
da 'ya'yansa maza goma sha biyar, da bayi ashirin. Suka ruga zuwa Urdun, inda

sarki yake. 18 Suka haye a mashigin don su ƙetaro da iyalin sarki, su kuma yi duk
abin da yake so.

Sa'ad da Shimeyi ɗan Gera ya haye Urdun, sai ya fāɗi rubda ciki a gaban sarki 19 ya
ce masa, "Ranka yă daɗe, ina roƙonka kada ka riƙe laifina a zuciya. Kada ka tuna da
laifin da na yi maka ranka yă daɗe, ranan nan da kake gudu daga Urushalima. Kada
ka tuna da shi ko kaɗan. 20 Na sani ni bawanka na yi maka laifi. Shi ya sa na zama
na farko daga dukan Gidan Yusuf, da mutanen Isra'ila wanda ya fito don yă tarye ka
yau, ranka yă daɗe, sarki."

21 Sai Abishai ɗan Zeruhiya ya ce, "Bai kamata a kashe Shimeyi saboda wannan
ba? Ya la'anci shafaffe na UBANGIJI."

22 Dawuda ya ce, "Me ya haɗa ni da ku, ku 'ya'yan Zeruhiya? Yau ɗin nan kun
zama maƙiyana! Ya kamata a kashe wani a Isra'ila a yau? Ban san cewa yau ni sarki
ne a bisa Isra'ila ba?" 23 Saboda haka sarki ya ce wa Shimeyi, "Ba za ka mutu ba."
Sarki kuwa ya yi alkawari har da rantsuwa.

24 Mefiboshet, jikan Shawulu, shi ma ya gangara don yă taryi sarki. Tun daga ranar
da sarki ya gudu har ran da ya komo lafiya, Mefiboshet bai lura da ƙafafunsa, ko yă
aske gemunsa, ko yă wanke tufafinsa ba. 25 Sa'ad da ya zo daga Urushalima don yă
taryi sarki, sai sarki ya ce masa, "Me ya sa ba ka tafi tare da ni ba Mefiboshet?"

26 Sai ya ce, "Ranka yă daɗe sarki, da yake bawanka gurgu ne, na ce, 'A sa mini
sirdi a kan jakina don in hau in tafi tare da sarki.' Amma Ziba bawana ya bashe ni.
27 Ya kuwa ɓata suna bawanka a gaban ranka yă daɗe, sarki. Ranka yă daɗe, sarki
yana kama da mala'ikan Allah, ka yi abin da ka ga ya fi maka kyau. 28 Duk zuriyar
kakana ba su cancanci kome ba sai mutuwa daga ranka yă daɗe, amma ka ba wa
bawanka wuri cikin mutanen da suke ci a teburinka. Saboda haka, wanda 'yanci
nake da shi da zan yi wani ƙarin roƙo a wurin sarki?"

29 Sarki ya ce masa, "Me ya sa kake zancen nan? Ai, na riga na umarta, da kai, da
Ziba ku raba filayen."

30 Mefiboshet ya ce wa sarki, "Bari yă ɗauki kome, yanzu da ranka yă daɗe, sarki
ya dawo gida lafiya."

31 Barzillai mutumin Gileyad shi ma ya zo daga Rogelim don yă ƙetare Urdun tare
da sarki, yă kuma sallame shi daga can. 32 To, Barzillai fa tsoho ne, mai shekara
tamanin. Ya tanada wa sarki a lokaci da yake Mahanayim, gama shi attajiri ne.
33 Sarki ya ce wa Barzillai, "Ka ƙetaro tare da ni ka zauna tare da ni a Urushalima,
zan kuwa tanada maka."

34 Amma Barzillai ya ce wa sarki, "Shekara nawa ya rage mini har da zan tafi
Urushalima da sarki? 35 Yanzu ina da shekara tamanin. Zan iya bambanta abu mai
daɗi da marar daɗi kuma ne? Bawanka zai iya jin ɗanɗano abin da yake ci, ko yake
sha ne? Har yanzu zan iya jin muryoyin mawaƙan maza da mata? Don me bawanka
zai zama ƙari kaya ga ranka yă daɗe? 36 Bawanka zai ƙetare Urdun tare da sarki,
yă ɗan yi maka rakiya kaɗan. Me ya sa ranka yă daɗe zai ba ni irin wannan lada.
37 Ka bar bawanka yă koma, don in mutu a garina, kusa da kabarin mahaifina da
mahaifiyata. Amma ga bawanka Kimham. Bari yă ƙetare tare da ranka yă daɗe,
sarki. Ka yi abin da ka ga dama da shi."

38 Sarki ya ce, "Kimham zai ƙetare tare da ni, zan kuwa yi masa abin da ya gamshe
ka. Kuma duk abin da kake bukata a wurina, zan yi maka."

39 Saboda haka dukan mutane suka ƙetare Urdun, sa'an nan kuma sarki ma ya
ƙetare. Sarki ya yi wa Barzillai sumba ya albarkace shi, sa'an nan Barzillai ya koma
gidansa.

40 Sa'ad da sarki ya ƙetare zuwa Gilgal, Kimham ma ya ƙetare tare da shi. Dukan
sojojin Yahuda da rabin sojojin Isra'ila suka ƙetare da sarki.

41 Nan take sai ga mutane Isra'ila suna zuwa wurin sarki, suna cewa, "Don me
'yan'uwanmu, mutanen Yahuda, suka saci sarki, suka kawo shi da iyalinsa a ƙetaren
Urdun, tare da dukan mutanensa?"
42 Dukan mutanen Yahuda suka ce wa mutanen Isra'ila, "Mun yi haka domin sarki
danginmu na kurkusa ne. Don me kuke fushi game da wannan? Mun ci wani abu
daga cikin kayan sarki ne? Mun ɗauki wani abu wa kanmu ne?"
43 Sa'an nan mutanen Isra'ila suka ce wa mutanen Yahuda, "Muna da rabo goma a
wurin sarki; ban da haka ma, muna da hakki mafi yawa a wurin Dawuda fiye da ku.
Don me kuke mana reni? Ba mu ne ma muka fara magana dawowa da sarki ba?"
Amma mutanen Yahuda suka ɗauka maganar da zafi fiye da mutanen Isra'ila.

# 20

*Sheba ya yi wa Dawuda tawaye*

1 Akwai wani mai tā-da-na-zaune-tsaye, sunansa Sheba, ɗan Bikri, daga kabilar
Benyamin, a wurin. Sai ya busa ƙaho, ya yi ihu ya ce,

"Ba mu da rabo a wurin Dawuda,
ba mu da sashe a wurin ɗan Yesse!
Kowa yǎ nufi tentinsa, ya Isra'ila!"

2 Saboda haka dukan mutane Isra'ila suka bar Dawuda don su bi Sheba ɗan Bikri.
Amma mutanen Yahuda suka kasance a wurin sarki tun daga Urdun har zuwa
Urushalima.
3 Da Dawuda ya komo fadarsa a Urushalima, sai ya ɗauko ƙwarƙwaran goma nan
da ya bari su lura da fada, ya keɓe su a wani gida inda za a yi tsaronsu. Ya tanada
musu, amma bai kwana da su ba. Aka sa su a keɓe har iyakar rayuwarsu, suka yi
zama kamar gwauraye.
4 Sa'an nan sarki ya ce wa Amasa, "Ka tattaro mutanen Yahuda su zo wurina cikin
kwana uku, kai kuwa ka kasance a can kai kanka." 5 Amma da Amasa ya tafi kiran
mutanen Yahuda, ya ɗauki lokaci fiye da lokacin da sarki ya ba shi.
6 Dawuda ya ce wa Abishai, "Ina gani Sheba ɗan Bikri zai ba mu wuya fiye da
Absalom. Ka ɗauki mutanen maigidanka ka fafare shi, don kada yǎ sami garuruwa
masu katanga yǎ tsere mana." 7 Saboda haka mutanen Yowab da Keretawa da
Feletiyawa da dukan jarumawa suka fita a ƙarƙashin Abishai. Suka fita daga
Urushalima don su fafari Sheba ɗan Bikri.
8 Yayinda suke a babban dutse a Gibeyon, Amasa ya zo don yǎ tarye su. Yowab
kuwa yana sanye da doguwar rigar soja, a ɗamarar da ya sha kuwa akwai wuƙa a
cikin kube. Da ya zo gaba sai wuƙar ta zāre daga kube ta fāɗi.
9 Yowab ya ce wa Amasa, "Yaya kake, ɗan'uwana?" Sai Yowab ya kama gemun
Amasa da hannun dama don yǎ yi masa sumba. 10 Amasa kuwa bai lura da wuƙar da
take hannun Yowab ba, Yowab kuwa ya soke shi da wuƙar a ciki, hanjinsa suka zube
ƙasa. Ba tare da ƙarin suƙa ba, Amasa ya mutu. Sa'an nan Yowab da ɗan'uwansa
Abishai suka fafari Sheba ɗan Bikri.
11 Ɗaya daga cikin mutanen Yowab ya tsaya kusa da Amasa ya ce, "Duk mai son
Yowab, kuma duk mai son Dawuda, yǎ bi Yowab!" 12 Amasa kuwa yana kwance cikin
tafkin jininsa a kan hanya, sai mutumin ya ga dukan sojoji suka zo suka tsaya cik a
can. Da ya gane cewa duk wanda ya haura zuwa wurin Amasa sai ya tsaya, sai ya ja
gawar Amasa daga hanyar ya kai can cikin wani fili ya rufe shi da zane. 13 Bayan an
ɗauke Amasa daga hanya, sai dukan mutane suka bi Yowab don fafaran Sheba ɗan
Bikri.

14 Sheba ya bi ta dukan kabilan Isra'ila zuwa Abel* da kuma ta dukan yankin
Beriyawa, waɗanda suka taru suka bi shi. 15 Sai dukan rundunonin da suke tare da
Yowab suka zo suka yi wa Sheba kwanton ɓauna a Abel-Bet-Ma'aka. Suka tara ƙasa
kewaye da jikin katangar birnin daidai da tsayinta. Sa'an nan waɗansu kuma suna
ƙoƙarin rushe katangar. 16 Sai wata mata mai hikima ta yi kira daga ciki birnin ta ce,
"Ku saurara! Ku saurara! Ku gaya wa Yowab yǎ zo nan ina so in yi magana da shi."
17 Ya tafi wurinta, sai ta ce, "Kai ne Yowab?"

Ya ce, "Ni ne".

Ta ce, "Ka ji abin da zan ce maka."

Ya ce, "Ina jinki."

18 Ta ci gaba ta ce, "A dā can, akan ce, 'Sami amsarka a Abel,' shi ke nan an gama.
19 Mu ne masu salama da kuma amintattu na Isra'ila. Kana ƙoƙari ka hallaka birnin
da yake uwa a Isra'ila. Don me kake so ka hallakar da gādon UBANGIJI?"

20 Yowab ya ce, "Allah yǎ sawwaƙe! Allah yǎ sawwaƙe in hallaka, ko in lalace
gādon UBANGIJI. 21 Ba haka ba ne batun. Wani mai suna Sheba ɗan Bikri ne, daga
ƙasar tudun Efraim, ya tayar wa sarki, yana gāba da Dawuda. Ki ba mu wannan
mutum, zan kuwa janye daga birnin."

Matar ta ce wa Yowab, "Za a jefa maka kansa daga katanga."

22 Sa'an nan matar ta tafi wurin dukan mutane da shawararta mai hikima, sai
suka datse kan Sheba ɗan Bikri suka jefa wa Yowab. Saboda haka sai ya busa ƙaho,
mutanensa kuwa suka watse daga birnin, kowa ya koma gidansa. Yowab kuma ya
koma wurin sarki a Urushalima.

23 Yowab ne yake shugabancin dukan rundunoni; Benahiya ɗan Yehohiyada ne
yake shugabancin Keretawa da Feletiyawa; 24 Adoniram kuwa shi ne shugaban aikin
gandu; Yehoshafat ɗan Ahilud shi ne marubucin tarihi; 25 Shewa kuwa magatakarda;
Zadok da Abiyatar su ne firistoci; 26 Ira mutumin Yayir kuwa shi ne firist na Dawuda.

# 21

*Gibeyonawa sun rama*

1 Lokacin da Dawuda yake mulki, an yi yunwa shekara uku a jere; saboda haka
Dawuda ya nemi nufin UBANGIJI. UBANGIJI ya ce, "Saboda Shawulu ne da alhakin
jinin gidansa; domin ya kashe Gibeyonawa."

2 Sai sarki ya tattara Gibeyonawa ya yi musu magana. (To, Gibeyonawa ba sashen
Isra'ilawa ba ne, amma mutanen Amoriyawa ne da suka ragu, waɗanda Isra'ila ta
rantse za tǎ bari da rai, amma Shawulu cikin kishinsa don Isra'ila da Yahuda ya yi
ƙoƙari yǎ hallaka su duka.) 3 Dawuda ya ce wa Gibeyonawa, "Me zan yi muku? Yaya
zan yi kafara domin ku sa wa masu gādon UBANGIJI albarka?"

4 Gibeyonawa suka ce, "Ba mu da 'yanci mu nemi zinariya ko azurfa daga wurin
Shawulu ko gidansa, ba mu kuwa da wani 'yanci mu sa a kashe wani a Isra'ila."

Dawuda ya ce, "To, me kuke so in yi muku?"

5 Suka ce wa sarki, "Mutumin da ya hallaka mu ya kuma yi mana makirci don
kada mu kasance tare da Isra'ilawa ko'ina a cikin ƙauyukansu, 6 a ba mu zuriyarsa
maza bakwai, mu kashe su, mu kuma rataye jikunansu a gaban UBANGIJI a Gibeya na
Shawulu wannan zaɓaɓɓen UBANGIJI."

Sai sarki ya ce, "Zan ba ku su."

7 Sarki ya ware Mefiboshet ɗan Yonatan jikan Shawulu, saboda rantsuwar da take
tsakanin Dawuda da Yonatan, ɗan Shawulu a gaban UBANGIJI. 8 Amma sarki ya
ɗauki Armoni da Mefiboshet, 'ya'ya biyu maza waɗanda Rizfa 'yar Aiya ta haifa
wa Shawulu, tare da 'ya'ya maza biyar na Merab 'yar Shawulu, waɗanda ta haifa

* 20:14 Ko kuwa Abel, har Bet Ma'aka; haka ma a aya 15.

wa Adriyel ɗan Barzillai, mutumin Mehola. 9 Ya ba da su ga Gibeyonawa, waɗanda
suka kashe su, suka kuma rataye jikunansu a gaban UBANGIJI. Dukan bakwai ɗin an
kashe su gaba ɗaya; an kashe su a farkon kwanankin girbi, daidai lokacin fara girbin
sha'ir.
10 Rizfa 'yar Aiya ta ɗauki tsumma ta yi wa kanta shimfiɗa a kan dutse. Tun daga
farkon girbi har ruwa damina ya sauko a kan gawawwakin, ba tă yarda tsuntsayen
sama su taɓa su da rana ko mugayen namun jeji da dare ba. 11 Da aka gaya wa
Dawuda abin da Rizfa 'yar Aiya ƙwarƙwaran Shawulu ta yi, 12 sai ya je ya kwashe
ƙasusuwan Shawulu da na ɗansa Yonatan daga mutanen Yabesh Gileyad (Gama
mutanen sun saci gawawwakin Shawulu da Yonatan daga inda Filistiyawa suka
kakkafa su a kan itace a filin Bet-Shan, bayan da Filistiyawa suka kashe su a Gilbowa.)
13 Dawuda ya kawo ƙasusuwan Shawulu da na ɗansa Yonatan daga can, a kuma aka
tattara dukan ƙasusuwan waɗanda Gibeyonawan suka kashe, suka kuma rataye.
14 Suka binne ƙasusuwan Shawulu da na ɗansa Yonatan a kabarin Kish, mahaifin
Shawulu, a Zela a Benyamin. Suka kuma yi kome da sarki ya umarta. Bayan wannan
Allah ya ji addu'arsu a madadin ƙasar.

*Yaƙe-yaƙe a kan Filistiyawa*
*(1 Tarihi 20.4-8)*

15 Har yanzu yaƙi ya sāke ɓarke tsakanin Filistiyawa da Isra'ila. Sai Dawuda ya
gangara tare da mutanensa don su yaƙi Filistiyawa, gajiya ta kama shi. 16 Ishbi-Benob
kuwa, wani daga zuriyar Rafa, wanda nauyin kan māshinsa na tagulla ya yi shekel
ɗari uku, wanda yake kuma da sabon māshi, ya ce zai kashe Dawuda. 17 Amma
Abishai ɗan Zeruhiya ya kawo wa Dawuda gudummawa; ya bugi Bafilistin, ya kashe
shi. Sa'an nan mutanen Dawuda suka rantse masa suka ce, "Ba za ka ƙara fita tare
da mu wurin yaƙi ba, don kada fitilar Isra'ila tă mutu."
18 Ana nan, sai aka sāke yin wani yaƙin da Filistiyawa, a Gob. A lokacin Sibbekai
mutumin Husha ya kashe Saf, wani daga zuriyar Rafa.
19 Sai aka sāke yin wani yaƙin da Filistiyawa a Gob, Elhanan ɗan Ya'are-Oregim*
mutumin Betlehem ya kashe Goliyat† mutumin Gat, wanda girmar sandan māshinsa
ta yi kama da taɓarya.
20 Har wa yau a wani yaƙin da aka yi a Gat, akwai wani ƙaton mutum mai yatsotsi
shida a kowane hannu, da kuma yatsotsi shida a kowane ƙafa, yatsotsi ashirin da
huɗu ke nan. Shi ma daga zuriya Rafa ne. 21 Da ya yi wa Isra'ila reni, sai Yonatan
ɗan Shimeya, ɗan'uwa Dawuda, ya kashe shi.
22 Waɗannan huɗu zuriyar Rafa ne a Gat, suka kuwa mutu ta hannu Dawuda da
mutanensa.

# 22

*Waƙar yabo da Dawuda ya yi*
*(Zabura 18.2-50)*

1 Dawuda ya rera wannan waƙa ga UBANGIJI, sa'ad da UBANGIJI ya cece shi daga
hannun dukan abokan gābansa, da kuma daga hannun Shawulu. 2 Ya ce,
"UBANGIJI shi ne dutsena, kagarata da kuma mai cetona;
3 Allahna shi ne dutsena. A gare shi nake samun kāriya
shi ne garkuwata da kuma ƙahon cetona.
Shi ne mafakata, maɓuyata, da mai cetona.
Daga mutane masu fitina, ka cece ni.

* **21:19** Ko kuwa ɗan Yayir mai saƙa. † **21:19** Ibraniyanci da Seftuwajin; 1Tar 20.5ɗan Yayir ya kashe Lahmi ɗan'uwan Goliyat

4 “Na kira ga UBANGIJI, wanda ya cancanci yabo,
na kuwa tsira daga abokan gābana.
5 Raƙumar ruwan mutuwa sun kewaye ni;
raƙumar ruwan hallaka suna cin ƙarfina.
6 Igiyoyin mutuwa sun nannaɗe ni;
tarkuna kuma suka auka mini.

7 “A cikin wahalata na yi kira ga UBANGIJI;
na yi kira ga Allahna.
Daga cikin haikalinsa ya saurare muryata;
kukata ta zo kunnensa.
8 Kasa ta yi rawa ta kuma girgiza,
harsashan sararin sama sun jijjigu;
suka yi makyarkyata saboda yana fushi.
9 Hayaƙi ya taso daga kafaffen hancinsa;
harshen wuta mai cinyewa daga bakinsa,
garwashi mai ƙuna daga bakinsa.
10 Ya buɗe sararin sama, ya sauko ƙasa,
girgije mai duhu suna ƙarƙashin ƙafafunsa.
11 Ya hau kerubobi, ya tashi sama;
ya yi firiya a fikafikan iska.
12 Ya mai da duhu abin rufuwarsa
gizagizai masu kauri cike da ruwa suka kewaye shi.
13 Daga cikin hasken gabansa
garwashi wuta mai ci ya yi walƙiya.
14 UBANGIJI ya yi tsawa daga sararin sama;
aka ji muryar Mafi Ɗaukaka.
15 Ya harbe kibiyoyi, ya wartsar da abokan gāba,
da walƙiya kuma ya sa suka gudu.
16 Aka bayyana kwarin teku,
tushen duniya suka tonu.
A tsawatawar UBANGIJI,
da numfashinsa mai ƙarfi daga hancinsa.

17 “Daga sama ya miƙo hannu ya ɗauke ni,
ya tsamo ni daga zurfafa ruwaye.
18 Ya kuɓutar da ni daga hannun abokin gāba mai iko,
daga maƙiyina da suka fi ƙarfina.
19 Suka auka mini cikin ranar masifata,
amma UBANGIJI ya kiyaye ni.
20 Ya fito da ni, ya kai ni wuri mafi fāɗi;
ya kuɓutar da ni gama yana jin daɗina.

21 “UBANGIJI ya sāka mini bisa ga adalcina;
bisa ga tsabtar hannuwana ya sāka mini.
22 Gama na kiyaye hanyoyin UBANGIJI;
ban yi wani mugun abu da zai juyar da ni daga Allahna ba.
23 Dukan dokokinsa suna a gabana;
ban ƙi ko ɗaya daga umarnansa ba.
24 Ba ni da laifi a gabansa
na kiyaye kaina daga yin zunubi.

25 UBANGIJI ya sāka mini bisa ga adalcina
bisa ga tsarkina a gabansa.

26 "Ga masu aminci, kakan nuna kanka mai aminci,
ga marasa laifi, kakan nuna kanka marar laifi,
27 ga masu tsarki, kakan nuna musu tsarki.
Amma ga masu karkataccen hali, kakan nuna kanka mai wayo.
28 Kakan ceci mai tawali'u,
amma idanunka suna a kan masu girman kai don ka ƙasƙantar da su.
29 Ya UBANGIJI kai ne fitilata;
UBANGIJI ya mai da duhuna haske.
30 Da taimakonka zan iya auka wa rundunar sojoji;
tare da Allahna zan iya hawan katanga.

31 "Ga Allah dai, hanyarsa cikakkiya ce;
maganar UBANGIJI babu kuskure.
Shi garkuwa ce
ga waɗanda suka nemi mafaka a gare shi.
32 Gama wane ne Allah, in ba UBANGIJI ba?
Wane ne dutse kuma in ba Allahnmu ba?
33 Allah ne ya ba ni ƙarfi,
ya kuma mai da hanyata cikakkiya.
34 Ya sa ƙafafuna kamar ƙafafun barewa;
ya sa na iya tsayawa a kan duwatsu.
35 Ya hori hannuwana don yaƙi,
hannuwana za su iya tanƙware bakan tagulla.
36 Ka ba ni garkuwar nasararka;
ka sauko don ka sa in sami girma.
37 Ka fadada hanya a ƙarƙashina
domin kada idon ƙafana yă juya.

38 "Na fafari abokan gābana, na murƙushe su;
ban kuwa juya ba sai da na hallaka su.
39 Na hallaka su ƙaƙaf, ba kuwa za su ƙara tashi ba,
sun fāɗi a ƙarƙashin sawuna.
40 Ka ba ni ƙarfi don yaƙi;
ka sa maƙiyina suka rusuna a ƙafafuna.
41 Ka sa abokan gābana suka juya a guje,
na kuwa hallaka maƙiyina.
42 Suka nemi taimako, amma babu wanda zai cece su,
suka yi kira ga UBANGIJI, amma ba a amsa musu ba.
43 Na murƙushe su, suka yi laushi kamar ƙura;
na daka na kuma tattake su kamar caɓi a kan rituna.

44 "Ka kuɓutar da ni daga harin mutanena;
ka kiyaye ni kamar shugaban al'ummai.
Mutanen da ban sansu ba za su kasance a ƙarƙashina,
45 baƙi kuma su na zuwa don su yi mini fadanci;
da zarar sun ji ni, sukan yi mini biyayya.
46 Zukatansu ta karaya;
suka fito da rawan jiki daga kagararsu.

47 "UBANGIJI yana a raye! Yabo ta tabbata ga Dutsena!
Ɗaukaka ga Allah, Dutse, Mai Cetona!
48 Shi ne Allahn da yake rama mini,
wanda ya sa al'ummai a ƙarƙashina,
49 wanda ya kuɓutar da ni daga maƙiyina.
Ka ɗaukaka ni bisa maƙiyina;
ka kiyaye ni daga hannun mugayen mutane.
50 Saboda haka, zan yabe ka, ya UBANGIJI cikin dukan al'ummai;
Zan rera waƙoƙin yabo ga sunanka.

51 "Ya ba wa sarkinsa kyakkyawan nasara;
ya nuna madawwamiyar ƙauna ga shafaffensa,
ga Dawuda da zuriyarsa har abada."

# 23

*Kalmomin Dawuda na ƙarshe*
1 Waɗannan su ne kalmomin Dawuda na ƙarshe.
"Abubuwan da Dawuda ɗan Yesse ya yi magana a kai,
abubuwan da mutumin da Mafi Ɗaukaka ya girmama.
Mutumin da Allah na Yaƙub ya zaɓa yǎ zama sarki,
wanda kuma yake mawaƙi waƙoƙin Isra'ila.*

2 "Ruhun UBANGIJI ya yi magana ta wurina;
maganarsa tana a harshena.
3 Allah na Isra'ila ya yi magana,
Dutsen Isra'ila ya ce mini,
'Sa'ad da wani ya yi mulkin mutane da adalci,
sa'ad da ya yi mulki da tsoron Allah,
4 yana kama da hasken safiya
a safiya marar girgije,
kamar haske bayan ruwan sama
da yakan sa ciyawa ta tsiro daga ƙasa.'

5 "Ashe, gidana bai daidaita da Allah ba?
Ashe, Allah bai yi madawwamiyar yarjejjeniya da ni
shiryayye da ɗaurarre a kowane sashi ba?
Ba zai kawo ga cikar cetona
yǎ kuma biya duk bukatuna ba?
6 Amma za a jefar da masu mugunta duka kamar ƙayayyuwan
da ba a tattara da hannu.
7 Duk wanda ya taɓa ƙaya
yakan yi amfani da wani ƙarfe ne ko sandar māshi;
akan ƙone su inda suke a zube."

*Jarumawan Dawuda*
*(1 Tarihi 11.10-19)*
8 Waɗannan su ne sunayen jarumawan Dawuda.

* **23:1** Ko kuwa Mawaƙin da Isra'ila suke ƙauna

Yosheb-Basshebet,† mutumin Takemon‡ ɗaya daga cikin shugabanni Uku; ya ɗaga māshinsa ya kashe mutum ɗari takwas§ a lokaci guda.
9 Na biye da shi a matsayi cikin jarumawa ukun nan, shi ne Eleyazar ɗan Dodo, mutumin Aho. Eleyazar ya kasance tare da Dawuda sa'ad da suka fuskanci Filistiyawa waɗanda suka taru a Fas Dammim don yaƙi. Mutanen Isra'ila suka gudu,
10 amma ya yi tsayi daka, ya bugi Filistiyawa sai da hannunsa ya gaji har ya liƙe wa māshinsa. UBANGIJI kuwa ya sa aka yi babban nasara a ranar. Sauran sojoji suka komo wurin Eleyazar, don kawai su washe ganima.
11 Na biye da Agiyi a matsayi, shi ne Shamma ɗan Agi, mutumin Harar. Sa'ad da Filistiyawa suka taru a wani wurin da take gona cike da waken barewa, sai rundunar Isra'ila suka gudu daga Filistiyawa. 12 Amma Shamma ya yi tsayi daka a tsakiyar gonar. Ya kāre ta, ya kuma bugi Filistiyawa, UBANGIJI kuwa ya sa aka yi babban nasara.
13 A lokacin girbi, uku daga cikin shugabanni talatin suka gangaro zuwa wurin Dawuda a kogon Adullam. A lokacin kuwa sojojin Filistiyawa sun kafa sansani a Kwarin Refayim. 14 Dawuda kuwa yana a mafaka. Wata ƙungiyar sojojin Filistiyawa kuma suna Betlehem. 15 Dawuda ya ji ƙishirwa, sai ya ce, "Kash, da a ce wani yǎ samo mini ruwa daga rijiyar da take kusa da bakin ƙofar Betlehem mana!" 16 Sai jarumawa ukun nan suka yi kukan ƙura, suka sheƙa a guje suka ratsa cikin sansanin Filistiyawa, suka ɗebo ruwa daga rijiyar da take kusa da bakin ƙofar Betlehem, suka kawo wa Dawuda. Amma Dawuda ya ƙi yǎ sha; a maimako sai ya zuba shi a gaban UBANGIJI. 17 Sai ya ce, "UBANGIJI yǎ sawwaƙe, in yi sha! Ba jinin mutanen da suka tafi a bakin ransu ba ne?" Dawuda kuwa bai sha ruwan ba.
Irin abubuwan da jarumawa ukun nan suka yi ke nan.

*(1 Tarihi 11.20-47)*

18 Abishai, ɗan'uwan Yowab, ɗan Zeruhiya shi shugaban Ukun nan.* Ya ɗauki māshinsa ya kashe mutane ɗari uku, ta haka ya zama sananne kamar Ukun nan.
19 Ashe, ba a girmama shi fiye da Ukun ba? Ya zama komandansu, ko da yake ba a haɗa shi a cikinsu ba.
20 Benahiya, ɗan Yehohiyada mutumin Kabzeyel shi ma jarumi ne sosai, ya yi nasarori masu yawa. Ya bugi ƙwararrun jarumawan Mowab guda biyu. Ya kuma shiga rami wata ranar da ake ƙanƙara, ya kashe zaki. 21 Ya kuma buge wani jibgaggen mutumin Masar. Duk da māshin da mutumin Masar yana riƙe a hannunsa, Benahiya ya kai masa hari da kulki. Ya ƙwace māshin daga hannunsa, ya kuma kashe shi da māshin. 22 Irin nasarorin da Benahiya ɗan Yehohiyada ya yi ke nan; shi ma jarumi ne sosai kamar jarumawan nan uku. 23 Aka fi ba shi girma fiye da talatin ɗin nan, amma ba ya cikin ukun. Dawuda ya sa shi yǎ zama ɗaya daga cikin masu tsaron lafiyarsa.

24 Cikin talatin ɗin kuwa akwai,

Asahel, ɗan'uwan Yowab,
Elhanan, ɗan Dodo mutumin Betlehem,
25 Shamma, mutumin Harod,
Elika, mutumin Harod,

---

† **23:8** Da Ibraniyanci; waɗansu rubuce-rubucen hannun Seftuwajin sun ba da ra'ayin cewa Ish-Boshet, wato, Esh-Ba'al (dubi kuma 1Tar 11.11Yashobeyam). ‡ **23:8** Mai yiwuwa wani sunan Bahakmone (dubi 1Tar 11.11). § **23:8** Waɗansu rubuce-rubucen hannun Seftuwajin (dubi kuma 1Tar 11.11); Rubuce-rubucen hannun Ibraniyanci da waɗansu rubuce-rubucen hannun Seftuwajin Uku; Adino Ba'ezni ne ya kashe mutum ɗari takwas
* **23:18** Yawancin rubuce-rubucen hannu na Ibraniyanci (dubi kuma 1Tar 11.20); biyu cikin rubuce-rubucen hannu na Ibraniyanci da Siriyak suna da Talatin ne a nan

[26] Helez, mutumin Falti,
Ira, ɗan Ikkesh mutumin Tekowa,
[27] Abiyezer, mutumin Anatot, da
Mebunnai,† mutumin Husha,
[28] Zalmon, mutumin Aho,
da Maharai, mutumin Netofa,
[29] Heleb,‡ ɗan Ba'ana daga Netofa,
Ittai, ɗan Ribai mutumin Gibeya a Benyamin,
[30] Benahiya, mutumin Firaton,
da Hiddai,§ daga rafuffukan Ga'ash,
[31] Abi-Albon, mutumin Arba, da
Azmawet, mutumin Bahurim,
[32] Eliyaba, mutumin Sha'albo,
'Ya'yan Yashen,
Yonatan, [33] ɗan* Shamma mutumin Harar,
da Ahiyam, ɗan Sharar† mutumin Harod.
[34] Elifelet, ɗan Ahasbai mutumin Ma'aka,
Eliyam, ɗan Ahitofel mutumin Gilo,
[35] Hezro, mutumin Karmel,
Fa'arai, mutumin Arbi,
[36] Igal, ɗan Natan mutumin Zoba,
ɗan Hagiri,‡
[37] Zelek, mutumin Ammon
Naharai, mutumin Beyerot mai ɗaukan wa Yowab, ɗan Zeruhiya makamai,
[38] Ira, mutumin Itra.
Gareb, mutumin Itra,
[39] da kuma Uriya, mutumin Hitti.

Su talatin da bakwai ne duka.

# 24

### *Dawuda ya ƙidaya mayaƙa*
### *(1 Tarihi 21.1-6)*

[1] Fushin UBANGIJI ya sāke ƙuna a kan Isra'ila, sai ya zuga Dawuda, yana cewa, "Je ka ƙidaya Isra'ila da Yahuda."

[2] Saboda haka sarki ya ce wa Yowab da komandodin da suke tare da shi, "Tafi cikin dukan kabilan Isra'ila, daga Dan har zuwa Beyersheba, ku ƙidaya mayaƙa don in san yawansu."

[3] Amma Yowab ya ce wa sarki, "UBANGIJI Allahnka ya sa mayaƙan su ƙaru sau ɗari fiye da yadda suke, har ranka yă daɗe, sarki yă gani da idonsa. Me ya sa ranka yă daɗe, sarki yake so yă yi abu haka?"

[4] Duk da haka, maganar sarki ya rinjayi Yowab da komandodin soja, sai suka tashi daga gaban sarki, suka tafi su ƙirga mayaƙan Isra'ila.

---

† **23:27** Da Ibraniyanci; waɗansu rubuce-rubucen hannu na Seftuwajin (dubi kuma 1Tar 11.29) Sibbekai ‡ **23:29** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na Ibraniyanci da na Bulget (dubi kuma 1Tar 11.30); yawancin rubuce-rubucen hannu na Ibraniyanci suna da Heled ne a nan § **23:30** Da Ibraniyanci; waɗansu rubuce-rubucen hannu na Seftuwajin suna da (dubi kuma 1Tar 11.32) Hurai ne a nan * **23:33** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na Seftuwajin (dubi kuma 1Tar 11.34); Ibraniyanci ba shi da ɗan. † **23:33** Ibraniyanci; (duba kuma 1Tar 11.35); Sakar ‡ **23:36** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na Seftuwajin (dubi kuma 1Tar 11.38); Ibraniyanci Haggadi

5 Bayan suka ƙetare Urdun, sai suka yi sansani kusa da Arower, kudu da garin da
yake cikin kwari, sa'an nan suka ratsa ta wajen Gad, suka ci gaba zuwa Yazer. 6 Suka
tafi Gileyad ta yankin Tatim Hodshi, sa'an nan suka tafi Dan Ya'an, suka kuma yi
wajen kewaye Sidon. 7 Sa'an nan suka yi ta wajen kagarar Taya da dukan garuruwan
Hiwiyawa da Kan'aniyawa. A ƙarshe, suka ci gaba zuwa Beyersheba a Negeb na
Yahuda.
8 Bayan suka ratsa dukan ƙasashen, a ƙarshe suka koma Urushalima, bayan wata
tara da kwana ashirin.
9 Yowab ya ba wa sarki jimillar yawan mayaƙan. A Isra'ila akwai mutum dubu
ɗari takwas da za su iya riƙe takobi. A Yahuda kuwa mutum dubu ɗari biyar.

*(1 Tarihi 21.7-17)*

10 Bayan Dawuda ya ƙidaya mayaƙan, lamirinsa ya kāshe shi, sai ya ce wa Ubangiji,
"Ya Ubangiji na yi laifi ƙwarai a kan abin da na yi. Ina roƙonka ka gafarta wa
bawanka. Na yi wauta ƙwarai."
11 Kafin Dawuda yă tashi da safe kashegari, maganar Ubangiji ta riga ta zo wa
annabin nan Gad, mai duban nan na Dawuda. Ubangiji ya ce, 12 "Je ka faɗa wa
Dawuda, 'Ga abin da Ubangiji ya ce, ina ba ka zaɓi uku. Ka zaɓi ɗaya daga cikinsu
don in aikata maka shi.' "
13 Sai Gad ya zo wurin Dawuda ya ce masa, "Kana so a yi yunwa shekara uku a
ƙasarka? Ko kana so ka yi ta gudu a gaban abokan gābanka har wata uku? Ko
kuwa ka fi so a yi annoba kwana uku a ƙasarka? Yanzu, sai ka yi tunani, ka yanke
shawarar game da amsar da zan mayar wa wanda ya aiko ni."
14 Dawuda ya ce wa Gad, "Na shiga uku. Gara mu fāɗa a hannuwan Ubangiji gama
alherinsa da girma yake. Amma fa kada ka bar ni in fāɗa a hannun mutane."
15 Saboda haka Ubangiji ya aika da annoba a kan Isra'ila tun daga safe har zuwa
lokacin da aka ƙayyade, mutum dubu saba'in kuwa daga Dan zuwa Beyersheba suka
mutu. 16 Da mala'ikan Ubangiji ya miƙa hannunsa wajen Urushalima, don yă hallaka
ta, sai Ubangiji ya tsai da masifar, ya ce wa mala'ikan da yake wahal da mutane, "Ya
isa, ka janye hannunka." A lokacin kuwa Mala'ikan Ubangiji yana tsaye a masussukar
Arauna, mutumin Yebus.
17 Da Dawuda ya ga mala'ikan da ya bubbugi mutane, sai ya ce wa Ubangiji, "Ni
ne na yi zunubi, na kuma yi abin da ba daidai ba. Waɗannan tumaki ne kawai. Me
suka yi? Bari hukuncinka yă sauko a kaina da iyalina."

### *Dawuda ya gina bagadi.*

*(1 Tarihi 21.18–22.1)*

18 A ranar, Gad ya koma wurin Dawuda ya ce, "Ka tashi, ka tafi ka gina wa
Ubangiji bagade a masussukar Arauna, mutumin Yebus." 19 Saboda haka Dawuda
ya haura, yadda Ubangiji ya umarta ta wurin Gad. 20 Da Arauna ya hangi Dawuda
da mutanensa suna zuwa wajensa, sai ya fita a guje, ya je ya rusuna a gaban sarki.
21 Arauna ya ce, "Me ya sa ranka yă daɗe, sarki ya zo wajen bawansa?"

Dawuda ya ce, "Don in saya masussukarka, saboda in gina wa Ubangiji bagade don
a tsayar da annoban da suke a bisa mutane."
22 Arauna ya ce wa Dawuda, "Bari ranka yă daɗe, sarki yă ɗauki duk abin da ya ga
dama yă miƙa shi. Ga shanu, don hadaya ta ƙonawa, ga kuma kayan masussuka da
itacen shanu, don itace." 23 Dukan wannan, ranka yă daɗe, Arauna ya ba wa sarki.
Arauna ya kuma ce, "Bari Ubangiji Allahnka yă karɓa."
24 Amma sarki ya ce wa Arauna, "A'a, dole in biya ka saboda waɗannan. Ba yadda
zan miƙa wa Ubangiji Allahna hadayun ƙonawa da bai ci mini kome ba."

Sai Dawuda ya saya, ya kuma biya masussukar, da shanun a bakin shekel hamsin
na azurfa. 25 Dawuda ya gina wa Ubangiji bagade a wurin, ya kuma miƙa masa

hadaya ta ƙonawa, da hadaya ta salama. Sa'an nan UBANGIJI ya amsa addu'o'in a madadin ƙasar, aka kuma kawar wa Isra'ila annoban.

# 1 Sarakuna

*Adoniya ya naɗa kansa Sarki*

1 Sa’ad da Sarki Dawuda ya tsufa ya kuma ƙara shekaru, ba ya iya jin ɗumi ko an
rufe shi da abin rufuwa. 2 Saboda haka bayinsa suka ce masa, “Bari mu nemi wata
budurwa wadda za tă yi wa ranka yă daɗe, sarki hidima, tă kuma kula da shi. Za tă
dinga kwanta kusa da ranka yă daɗe, yă ji ɗumi.”

3 Suka nemi kyakkyawar yarinya cikin fāɗin Isra’ila, sai suka sami Abishag,
mutuniyar Shunam, suka kawo ta wa sarki. 4 Yarinyar kuwa kyakkyawa ce ƙwarai;
ta kuwa lura da sarki, ta kuma yi masa hidima, amma sarki bai yi jima’i da ita ba.

5 Adoniya,* wanda mahaifiyarsa ce Haggit, ya fito ya ce, “Zan zama sarki.” Saboda
haka ya nemi kekunan yaƙi, ya kuma shirya dawakai, tare da mutane hamsin da za
su sha gabansa. 6 (A duk rayuwarsa mahaifinsa bai taɓa tsawata masa yă ce, “Me ya
sa kake yin haka ba?” Shi kuwa mai kyan gani ne ƙwarai, shi ne aka haifa bayan
Absalom.)

7 Adoniya ya haɗa baki da Yowab ɗan Zeruhiya† da kuma Abiyatar firist, suka kuma
ba shi goyon baya. 8 Amma Zadok firist, Benahiya ɗan Yehohiyada, annabi Natan,
Shimeyi, Reyi‡ da kuma matsara na musamman na Dawuda ba su bi Adoniya ba.

9 Wata rana Adoniya ya tafi Dutsen Zohelet kusa da En Rogel, inda ya yi hadayar
tumaki, da shanun noma, da shanun da ake kiwo a gida. Ya kuma gayyaci
’yan’uwansa, wato, sauran ’ya’yan Sarki Dawuda, tare da dukan dattawan sarki da
suka fito daga Yahuda, 10 amma bai gayyaci annabi Natan, ko Benahiya, ko wani daga
matsara na musamman, ko kuwa ɗan’uwansa Solomon ba.

11 Sai Natan ya ce wa Batsheba, mahaifiyar Solomon, “Ki san cewa Adoniya, ɗan
Haggit, ya zama sarki ba tare da sanin ranka yă daɗe, sarkinmu Dawuda ba? 12 Yanzu
bari in ba ki shawara yadda za ki cece ranki da kuma ran ɗanki Solomon. 13 Ki
shiga wurin Sarki Dawuda ki ce masa, ‘Ranka yă daɗe sarki, ba ka rantse mini ni
baiwarka cewa, “Tabbatacce Solomon ɗanka ne zai zama sarki bayana, yă kuma
zauna a kujerar sarautar ba”? To, me ya sa Adoniya ya zama sarki?’ 14 Yayinda kike
can kina magana da sarki, zan shiga in kuma tabbatar da abin da kika faɗa.”

15 Saboda haka Batsheba ta je don tă ga sarki. A yanzu dai sarki ya tsufa, yana nan
kuma a cikin ɗakinsa, inda Abishag mutuniya Shunam take masa hidima. 16 Batsheba
ta rusuna ta kuma durƙusa a gaban sarki.

Sai sarki ya tambaye ta ya ce, “Me kike so?”

17 Ta ce masa, “Ranka yă daɗe, kai kanka ka rantse mini ni baiwarka da sunan
Ubangiji Allahnka cewa, ‘Solomon ɗanka zai zama sarki bayana, zai kuma zauna a
kujerar sarautata.’ 18 Amma yanzu Adoniya ya zama sarki, kai kuwa ranka yă daɗe
sarki, ba ka san wani abu game da shi ba. 19 Ya miƙa hadayun shanu, da shanun da
ake kiwo a gida, da tumaki masu yawa, ya kuma gayyaci dukan ’ya’yan sarki maza,
da Abiyatar firist, da Yowab shugaban mayaƙa, amma bai gayyaci Solomon bawanka
ba. 20 Ranka yă daɗe sarki, idanun dukan Isra’ila suna a kanka, domin su san wa zai
zauna a kujerar ranka yă daɗe sarkina, a bayanka. 21 In ba haka, bayan an binne
ranka yă daɗe sarki, tare da kakanninsa, za a wulaƙance ni da Solomon ɗana, kamar
masu laifi.”

---

* **1:5** Adoniya shi ne ɗa na huɗu na Dawuda (2Sam 3.4) kuma yana da shekara 35 da haihuwa. Amnon, Absalom, da Kileyab (da ya mutu yana yaro) duk sun mutu. † **1:7** Zeruhiya ’yar’uwar Dawuda ce ‡ **1:8** Ko kuwa da abokansa

22 Yayinda take cikin magana tare da sarki, sai annabi Natan ya iso. 23 Sai aka faɗa
wa sarki, “Ga annabi Natan.” Da Natan ya je gaban sarki, sai ya rusuna da fuskarsa
har ƙasa.
24 Natan ya ce, “Ranka yă daɗe, sarki, ko ka furta cewa Adoniya ne zai zama sarki
a bayanka, yă kuma zauna a kujerar sarautarka? 25 Yau ya gangara, ya kuma miƙa
hadayun shanu, da shanun da ake kiwo a gida, da tumaki masu yawa. Ya gayyaci
dukan ’ya’yan sarki maza, da shugaban mayaƙa, da kuma Abiyatar firist. A yanzu
haka suna ci, suna sha, tare da shi, suna cewa, ‘Ran Sarki Adoniya yă daɗe!’ 26 Amma
bai gayyace ni bawanka, da Zadok firist, da Benahiya ɗan Yehohiyada, da kuma
bawanka Solomon ba. 27 Ranka yă daɗe, sarki, ko ka tabbatar da haka, amma ba
ka ko faɗa wa fadawanka, cewa ga wanda zai gāje Ranka yă daɗe, sarki ba?”

### *Dawuda ya naɗa Solomon Sarki*

28 Sai Dawuda ya ce, “Kira Batsheba tă shiga.” Sai ta zo gaban sarki ta kuma tsaya
a gabansa.
29 Sai sarki ya yi rantsuwa, “Muddin UBANGIJI yana a raye, wanda ya cece ni daga
kowace damuwa, 30 tabbatacce a yau zan aikata abin da na yi miki rantsuwa da sunan
UBANGIJI, Allah na Isra’ila; Solomon ɗanki zai zama sarki bayana, kuma shi zai zauna
a kan kujerar sarautata a maimakona.”
31 Sai Batsheba ta rusuna da fuskarta har ƙasa, ta kuma durƙusa a gaban sarki ta
ce, “Bari ran Sarkina Dawuda yă daɗe, har abada!”
32 Sarki Dawuda ya ce, “Ku kira mini Zadok firist, annabi Natan, da Benahiya ɗan
Yehohiyada.” Da suka zo gaban sarki, 33 sai ya ce musu, “Ku ɗauki bayin sarki tare da
ku, ku kuma sa ɗana Solomon a kan dokina, ku gangara da shi zuwa Gihon. 34 A can
ku sa Zadok firist, da annabi Natan su shafe shi sarki a bisa Isra’ila. Ku busa ƙaho,
ku kuma yi ihu, kuna cewa, ‘Ran Sarki Solomon yă daɗe!’ 35 Sa’an nan ku haura tare
da shi, zai kuwa zo yă zauna a kujera sarautata, yă yi mulki a maimakona. Na naɗa
shi mai mulki a bisa Isra’ila da Yahuda.”
36 Benahiya ɗan Yehohiyada ya amsa wa sarki, ya ce, “Amin! Bari UBANGIJI Allah na
ranka yă daɗe sarkina, yă tabbatar da haka. 37 Kamar yadda UBANGIJI ya kasance da
ranka yă daɗe, sarki, haka ma bari yă kasance da Solomon, yă kuma mai da kujerar
sarautarsa tă fi kujerar sarautar ranka yă daɗe, Sarki Dawuda, girma!”
38 Sai Zadok firist, annabi Natan, Benahiya ɗan Yehohiyada, Keretawa, da
Feletiyawa suka gangara, suka sa Solomon a kan dokin Sarki Dawuda, suka raka
shi zuwa Gihon. 39 Zadok firist ya ɗauki ƙahon mai daga tenti mai tsarki, ya shafe
Solomon. Sa’an nan suka busa ƙaho, sai dukan mutane suka yi ihu, suna cewa “Ran
Sarki Solomon yă daɗe!” 40 Dukan mutane kuwa suka haura suka bi shi, suna busan
sarewa, suna farin ciki sosai, har ƙasa ta girgiza saboda sowa.
41 Adoniya tare da dukan baƙin da suke tare da shi kuwa suka ji wannan sa’ad da
suke gama bikinsu. Da jin busan ƙaho, sai Yowab ya yi tambaya, ya ce, “Me ya jawo
surutu haka a birni?”
42 Tun yana cikin magana, sai Yonatan ɗan Abiyatar ya iso. Adoniya ya ce, “Shigo!
Ai, mutumin kirki irinka, lalle ka kawo labari mai daɗi ne.”
43 Yonatan ya ce wa Adoniya, “A ina! Ranka yă daɗe, Sarkinmu Dawuda ya naɗa
Solomon sarki. 44 Sarki ya aika shi tare da Zadok firist, annabi Natan, Benahiya ɗan
Yehohiyada, Keretawa, da Feletiyawa, suka sa shi a kan dokin sarki, 45 Zadok firist
kuwa da annabi Natan sun shafe shi sarki a Gihon. Daga can suka haura suna kirari,
birni kuwa ta ɓarke da sowa. Surutun da kake ji ke nan. 46 Ban da haka ma, Solomon
ne sarki yanzu. 47 Yanzu haka, fadawa sun zo suna wa ranka yă daɗe, Sarki Dawuda,
sam barka, suna cewa, ‘Bari Allahnka yă sa sunan Solomon yă zama sananne fiye da
naka, bari kuma sarautarsa tă fi taka girma!’ Sarki kuwa ya rusuna, ya yi sujada a

kan gadonsa [48] ya ce, ‘Yabo ga UBANGIJI, Allah na Isra’ila, wanda ya bar idanuna suka
ga magāji a kan kujerar sarautata a yau.’ ”
[49] A nan fa, dukan baƙin Adoniya suka taso da rawar jiki suka watse. [50] Amma
Adoniya, don tsoron Solomon, ya je ya kama ƙahon bagade ya riƙe. [51] Sa’ad da aka
faɗa wa Solomon cewa, “Adoniya yana tsoron Sarki Solomon, kuma ya manne wa
ƙahonin bagade. Yana cewa, ‘Bari Sarki Solomon yă rantse mini a yau cewa ba zai
kashe bawansa da takobi ba.’ ”
[52] Solomon ya amsa ya ce, “In ya nuna kansa mai biyayya, ba gashin kansa da zai
fāɗi ƙasa; amma in aka same mugunta a cikinsa, zai mutu.” [53] Sai Sarki Solomon ya
aiki mutane, suka kuma sauko da shi daga bagade. Adoniya kuwa ya zo, ya rusuna
wa Sarki Solomon, sai Solomon ya ce, “Tafi gidanka.”

# 2

### *Dawuda ya gargaɗe Solomon*

[1] Da lokacin mutuwar Dawuda ya yi kusa, sai ya gargaɗe Solomon ɗansa, ya ce,
[2] “Ina gab da bin hanyar da kowa a duniya zai bi. Saboda haka ka yi ƙarfin hali, ka
nuna kanka namiji, [3] ka kiyaye abin da UBANGIJI Allahnka yake bukata. Yi tafiya a
hanyoyinsa, ka kiyaye ƙa’idodi, da umarnai, da dokoki, da kuma farillansa, kamar
yadda suke a rubuce a Dokar Musa, don ka yi nasara a cikin kome da za ka yi, da
kuma inda za ka tafi. [4] UBANGIJI kuwa zai kiyaye alkawarinsa gare ni da ya ce, ‘In
zuriyarka suka lura da yadda suke rayuwa, in kuma suka yi tafiya da aminci a gabana
da dukan zuciyarsu, da kuma dukan ransu, ba za ka kāsa samun mutum a kujerar
sarautar Isra’ila ba.’
[5] “Yanzu fa, kai kanka ka san abin da Yowab ɗan Zeruhiya ya yi mini. Abin da ya
yi wa shugabanni biyun nan na mayaƙan Isra’ila, wato, Abner ɗan Ner, da Amasa
ɗan Yeter. Ya kashe su, ya kuma zub da jininsu a lokacin salama sai ka ce a fage yaƙi,
da wannan jini ya yi ɗamara a gindinsa, ya kuma sa takalma a ƙafafunsa. [6] Ka yi da
shi gwargwadon hikimarka, amma kada ka bari yă gangara kabari da furfura* cikin
salama.
[7] “Amma ka yi alheri ga ’ya’yan Barzillai mutumin Gileyad, ka sa su kasance a cikin
waɗanda suke ci a teburinka. Sun goyi bayana sa’ad da nake gudu daga ɗan’uwanka
Absalom.
[8] “Ka tuna, akwai kuma Shimeyi ɗan Gera, mutumin Benyamin daga Bahurim,
wanda ya yi ta yin mini muguwar la’ana a ranar da na tafi Mahanayim. Sa’ad da ya
gangara ya same ni a Urdun, na rantse masa da sunan UBANGIJI na ce, ‘Ba zan kashe
ka da takobi ba.’ [9] Amma yanzu, kada ka ɗauke shi marar laifi. Kai mutum ne mai
hikima; za ka san abin da za ka yi da shi. Ka kawo furfuransa zuwa kabari da jini.”
[10] Sa’an nan Dawuda ya huta tare da kakanninsa. Sai aka binne shi a Birnin
Dawuda. [11] Ya yi sarauta shekaru arba’in a bisa Isra’ila. Wato, shekaru bakwai a
Hebron da kuma talatin da uku a Urushalima. [12] Solomon kuwa ya zauna a kan
kujerar sarautar mahaifinsa Dawuda, mulkinsa kuwa ya kahu sosai.

### *Sarautar Solomon ta kahu*

[13] To, sai Adoniya, ɗan Haggit ya tafi wurin Batsheba mahaifiyar Solomon. Ita kuwa
ta tambaye shi ta ce, “Lafiya?”
Ya amsa ya ce, “I, lafiya.” [14] Sa’an nan ya ƙara da cewa, “Ina da ɗan wani abin da
zan faɗa miki.”
Ta ce, “Faɗa.”
[15] Sai ya ce, “Kamar yadda kika sani, mulkin nan nawa ne. Dukan Isra’ila suna
ɗaukana a matsayin sarki. Amma abubuwa suka canja, sai mulkin ya koma ga

* **2:6** Da Ibraniyanci Sheol; haka ma a aya 9.

ɗan'uwana; gama ya zo masa daga UBANGIJI ne. 16 Yanzu ina da roƙo guda da zan yi
gare ki. Kada ki hana mini."

Ta ce, "Sai ka faɗa."

17 Sai ya ci gaba, "In kin yarda, ki yi magana da Sarki Solomon, gama ba zai ƙi jinki
ba, ki ce yă ba ni yarinyan nan, Abishag, mutuniyar Shunam, tă zama matata."

18 Batsheba ta ce, "Da kyau, zan yi magana da sarki dominka."

19 Sai Batsheba ta tafi wurin Sarki Solomon don tă yi masa magana a kan Adoniya.
Sarki ya miƙe tsaye don yă sadu da ita, ya rusuna mata, ya kuma zauna a kujerar
sarautarsa. Ya sa aka kawo wa mahaifiyar sarki kujerar sarauta, ta kuwa zauna a
gefen damansa.

20 Ta ce, "Ina da ɗan roƙon da zan nema ka yi mini. Ina fata ba za ka hana ni ba."

Sai sarki ya amsa ya ce, "Mahaifiyata, sai ki faɗa in ji, ba zan hana miki ba."

21 Saboda haka sai ta ce, "Ka sa a ba wa ɗan'uwanka Adoniya, Abishag mutuniyar
Shunam tă zama matarsa."

22 Sarki Solomon ya amsa wa mahaifiyarsa ya ce, "Me ya sa kika roƙar wa Adoniya
Abishag mutuniyar Shunam kawai? Ki ma sa a ba shi mulkin mana. Ai, shi yayana
ne. I, ki roƙa dominsa, da domin Abiyatar firist, da kuma domin Yowab ɗan Zeruhiya
mana!"

23 Sai Sarki Solomon ya rantse da sunan UBANGIJI ya ce, "Bari Allah yă yi mini
hukunci mai tsanani, idan ban sa Adoniya ya biya wannan roƙo da ransa ba! 24 Yanzu
kuwa, muddin UBANGIJI yana a raye, shi wanda ya kafa ni sosai a kan kujerar sarautar
mahaifina Dawuda, ya kuma kafa mini mulki kamar yadda ya yi alkawari; za a kashe
Adoniya yau!" 25 Saboda haka Sarki Solomon ya umarci Benahiya ɗan Yehohiyada
yă kashe Adoniya; ya kuwa kashe shi.

26 Ga Abiyatar firist kuwa sarki ya ce, "Tafi gonarka a Anatot. Ka cancanci ka mutu,
amma ba zan kashe ka yanzu ba, domin ka ɗauki akwatin alkawarin UBANGIJI Mai Iko
Duka a gaban mahaifina Dawuda, ka kuma sha wahala tare mahaifina." 27 Saboda
haka Solomon ya cire Abiyatar daga aikin firist na UBANGIJI, ya cika maganar da
UBANGIJI ya yi a Shilo game da gidan Eli.

28 Sa'ad da labarin ya kai wurin Yowab, wanda ya haɗa kai da Adoniya, ko da
yake bai haɗa kai da Absalom ba, sai ya gudu zuwa tentin UBANGIJI, ya kama
ƙahonin bagade ya riƙe. 29 Aka faɗa wa Sarki Solomon cewa Yowab ya gudu zuwa
tentin UBANGIJI, yana kuma kusa da bagade. Sai Solomon ya umarci Benahiya ɗan
Yehohiyada ya ce, "Je ka kashe shi!"

30 Sai Benahiya ya shiga tentin UBANGIJI ya ce wa Yowab, "Sarki ya ce, 'Ka fita!' "

Amma Yowab ya amsa ya ce, "A'a, a nan zan mutu."

Sai Benahiya ya ce wa sarki, "Ga yadda Yowab ya amsa mini."

31 Sai sarki ya umarci Benahiya ya ce, "Yi kamar yadda ya faɗa. Ka kashe shi,
ka kuma binne shi, ka wanke ni da gidan mahaifina daga laifin jini marasa laifin
da Yowab ya zubar. 32 UBANGIJI zai sāka masa saboda jinin da ya zubar, domin
ba da sanin mahaifina Dawuda ne ya fāɗa wa mutum biyun nan da takobi ba.
Dukansu biyu, Abner ɗan Ner, shugaban mayaƙan Isra'ila, da Amasa ɗan Yeter,
shugaban mayaƙan Yahuda, mutane ne mafi kyau da kuma mafi adalci fiye da shi.
33 Bari alhakin jininsu yă koma a kan Yowab da kuma zuriyarsa har abada. Amma
bari salamar UBANGIJI tă kasance a kan Dawuda da zuriyarsa, da gidansa, da kuma
mulkinsa, har abada."

34 Sai Benahiya ɗan Yehohiyada ya haura ya bugi Yowab, ya kashe shi, ya kuwa
binne shi a gidansa† a ƙauye. 35 Sai sarki ya sa Benahiya ɗan Yehohiyada ya zama
shugaba a bisa mayaƙa a matsayin Yowab, ya kuma sa Zadok firist a wurin Abiyatar.

† **2:34** Ko kuwa binne shi a kabarinsa

36 Sa'an nan sarki ya aika aka kawo Shimeyi, ya kuma ce masa, "Ka gina wa kanka
gida a nan a Urushalima, ka zauna a ciki, kada ka kuskura ka tafi wani wuri. 37 Gama
ran da ka fita, ka haye Kwarin Kidron, ka tabbata za ka mutu, alhakin jininka kuwa
zai koma kanka."
38 Shimeyi ya amsa wa sarki ya ce, "Abin da ka faɗa yana da kyau. Bawanka zai yi
kamar yadda ranka yă daɗe sarki, ya faɗa." Shimeyi kuwa ya yi zama a Urushalima
na dogon lokaci.
39 Amma bayan shekaru uku, biyu daga cikin bayin Shimeyi suka gudu zuwa wurin
Akish ɗan Ma'aka, sarkin Gat. Aka faɗa wa Shimeyi cewa, "Bayinka suna a Gat." 40 Da
jin haka, sai ya tashi ya shimfiɗa wa jakinsa abin zama, ya hau, ya tafi Gat wurin
Akish domin neman bayinsa. Shimeyi kuwa ya dawo da su gida daga Gat.
41 Da aka faɗa wa Solomon cewa Shimeyi ya bar Urushalima zuwa Gat, har ya
dawo. 42 Sai sarki ya aika a kawo Shimeyi, ya ce masa, "Ban sa ka rantse da sunan
UBANGIJI, na kuma ja maka kunne cewa, 'A ranar da ka kuskura ka bar nan ka tafi
wani wuri, ka tabbata za ka mutu ba'? A lokacin ka ce mini, 'Abin da ka faɗa yana da
kyau. Zan kuwa kiyaye.' 43 To, me ya sa ba ka kiyaye rantsuwar da ka yi ga UBANGIJI,
ka kuma yi biyayya da umarnin da na ba ka ba?"
44 Sarki ya ce wa Shimeyi, "Ka sani a zuciyarka dukan muguntar da ka yi wa
mahaifina Dawuda. Yanzu UBANGIJI zai sāka maka saboda muguntarka. 45 Amma
za a yi wa Sarki Solomon albarka, sarautar Dawuda kuma za tă kasance a tsare a
gaban UBANGIJI har abada."
46 Sai sarki ya umarci Benahiya ɗan Yehohiyada, yă fita, yă bugi Shimeyi, yă kashe
shi. Ya kuwa kashe shi.
Mulki kuwa ya kahu sosai a hannun Solomon.

# 3

### *Solomon ya nemi hikima*
### *(2 Tarihi 1.1-13)*

1 Solomon ya haɗa kai da Fir'auna sarkin Masar, ya kuwa auri 'yarsa. Ya kawo
ta cikin Birnin Dawuda kafin yă gama ginin fadarsa, da haikalin UBANGIJI, da kuma
katanga kewaye da Urushalima. 2 A lokacin dai mutane suna miƙa hadaya a wurare
a bisa tuddai, domin ba a riga an gina haikali saboda Sunan UBANGIJI ba. 3 Solomon
ya ƙaunaci UBANGIJI ta wurin yin tafiya bisa ga farillan mahaifinsa Dawuda, sai dai
ya miƙa hadayu, ya kuma ƙone turare a wuraren nan na bisa tuddai.
4 Sai sarki Solomon ya tafi Gibeyon don yă miƙa hadayu, gama a can ne wuri mafi
muhimmanci na sujada. Solomon kuwa ya miƙa hadayun ƙonawa guda dubu a kan
wannan bagade. 5 A Gibeyon, UBANGIJI ya bayyana ga Solomon da dare a mafarki,
Allah ya ce, "Ka roƙi abin da kake so in ba ka."
6 Solomon ya amsa ya ce, "Ka nuna alheri mai girma ga bawanka, mahaifina
Dawuda domin ya yi aminci gare ka da adalci, ya kuma kasance da zuciya mai
gaskiya. Ka ci gaba da wannan alheri mai girma gare shi, ka ba shi ɗa don yă zauna
a kujerar sarautarsa a wannan rana.
7 "Yanzu, ya UBANGIJI Allahna, ka sa bawanka a wurin mahaifina Dawuda. Amma
ni ɗan yaro ne kawai, ban kuma san yadda zan yi ayyukana ba. 8 Bawanka yana
nan a cikin mutanen da ka zaɓa, mutane masu girma, waɗanda suka wuce ƙirge,
ko a lissafta. 9 Saboda haka ka ba bawanka zuciyar ganewa, don yă shugabanci
mutanenka, yă kuma iya rarrabe tsakanin abin da yake daidai da abin da ba daidai
ba. Gama wa zai iya shugabance wannan mutanenka masu girma haka?"
10 Sai Ubangiji ya ji daɗi cewa Solomon ya roƙa wannan. 11 Saboda haka Allah ya ce
masa, "Da yake ka nemi wannan ne, ba ka kuwa nemi tsawon rai ko arziki wa kanka

ba, ba ka kuma nemi mutuwar abokan gābanka ba, amma ka nemi ganewa a aikata
gaskiya, 12 zan yi abin da ka roƙa. Zan ba ka zuciya mai hikima da ta ganewa, har yă
zama ba a taɓa samun wani kamar ka ba, ba kuwa za a taɓa samunsa ba. 13 Ban da
haka ma, zan ba ka abin da ba ka nema ba; arziki da girma, don a rayuwarka ba za ka
kasance da wani kamar ka ba a cikin sarakuna. 14 In kuma ka yi tafiya a hanyoyina,
ka kuma yi biyayya da farillaina da umarnaina kamar yadda Dawuda mahaifinka ya
yi, zan ba ka tsawon rai." 15 Sai Solomon ya farka, ya gane ashe mafarki ne.

Ya koma Urushalima, ya tsaya a gaban akwatin alkawarin Ubangiji ya miƙa hadayun ƙonawa da hadayun salama. Sa'an nan ya shirya wa fadawansa biki.

### *Shari'a mai hikima*

16 To, ana nan sai waɗansu karuwai biyu suka zo wurin sarki, suka tsaya a gabansa.
17 Sai ɗaya ta ce, "Ranka yă daɗe, wannan mata da ni muna zama a gida ɗaya.
Na haifi jariri yayinda take can tare da ni. 18 Kwana uku bayan haihuwar jaririna,
wannan mata ma ta haifi jariri. Mu dai kaɗai ne; babu wani a gidan sai mu biyu.

19 "Da dare ɗan wannan matan ya mutu domin ta kwanta a kansa. 20 Saboda haka
ta tashi da tsakar dare ta ɗauki ɗana daga gefena yayinda baiwarka take barci. Sai
ta sa shi kusa da ƙirjinta, ta kuma sa mataccen ɗanta kusa da ƙirjina. 21 Kashegari,
da na farka don in shayar da ɗana, sai na tarar ya mutu! Amma sa'ad da na dube
shi da kyau da safe, sai na ga ashe ba ɗan da na haifa ba ne."

22 Amma ɗaya matar ta ce, "A'a! Mai rai ɗin ne ɗana; mataccen naki ne."

Amma ta farin ta nace, "A'a! Mataccen ne naki; mai ran ne nawa." A haka suka yi ta gardama a gaban sarki.

23 Sarki ya ce, "Wannan ta ce, 'Ɗana ne a raye, naki ne matacce,' yayinda ɗayan
tana cewa, 'A'a! Ɗanki ne mataccen, nawa ne a raye.' "

24 Sai sarki ya ce, "Kawo mini takobi." Sai aka kawo takobi wa sarki. 25 Ya ba da
umarni ya ce, "Yanka yaron nan mai rai, gida biyu, kowacce ta ɗauki rabi."

26 Ainihin mamar ɗan da yake a raye ta cika da tausayi saboda ɗanta, sai ta ce wa
sarki, "Ina roƙonka, ranka yă daɗe, kada ka kashe yaron! Ka ba ta kawai!"

Amma ɗayan matar ta ce, "Kada a ba kowa daga cikinmu ɗan da rai, a ci gaba a raba shi!"

27 Sai sarki ya zartar da hukuncinsa ya ce, "A ba da jariri mai ran ga mata ta fari.
Kada a kashe shi; ita ce ainihin mahaifiyarsa."

28 Sa'ad da dukan Isra'ila suka ji hukuncin da sarki ya zartar, suka girmama sarki
sosai, domin sun gane cewa Allah ya ba shi hikimar yin shari'ar adalci.

# 4

### *Shugabanni da gwamnonin Solomon*

1 Sai Sarki Solomon ya yi mulki a bisa dukan Isra'ila.

2 Waɗannan su ne manyan shugabanninsa.

Azariya ɗan Zadok shi ne firist;
3 Elihoref da Ahiya, 'ya'yan Shisha maza, su ne marubuta.
Yehoshafat ɗan Ahilud, shi ne mai lura da takardu.
4 Benahiya ɗan Yehohiyada, shi ne shugaban mayaƙa.
Zadok da Abiyatar, su ne firistoci.
5 Azariya ɗan Natan, shi ne mai lura da shugabannin yanki.
Zabud ɗan Natan, shi ne firist da kuma mai wa sarki shawara.
6 Ahishar, shi ne sarkin fada.
Adoniram ɗan Abda, shi ne mai lura da aikin gandu.

7 Solomon yana da gwamnoni yankuna goma sha biyu a bisa dukan Isra'ila,
waɗanda suke tanaji abinci domin sarki da kuma gidan sarauta. Kowanne yakan
tanada abinci na wata ɗaya a shekara.

8 Ga sunayensu,

Ben-Hur, shi ne a ƙasar tudun Efraim;
9 Ben-Deker, shi ne a Makaz, Sha'albim, Bet-Shemesh da Elon Bet-Hanan;
10 Ben-Hesed, shi ne a Arubbot (Soko da dukan ƙasar Hefer);
11 Ben-Abinadab, shi ne a Nafot Dor (ya auri Tafat 'yar Solomon);
12 Ba'ana ɗan Ahilud, shi ne a Ta'anak da Megiddo, da kuma dukan Bet-Sheyan biye da Zaretan ƙasa da Yezireyel, daga Bet-Sheyan zuwa Abel-Mehola a ƙetaren Yokmeyam;
13 Ben-Geber, shi ne a Ramot Gileyad (Mazaunan Yayir ɗan Manasse a Gileyad suna a ƙarƙashinsa, haka ma yankin Argob a Bashan tare da manyan biranen sittin masu katanga da suke da ƙyamare na tagulla);
14 Ahinadab ɗan Iddo, shi ne a Mahanayim;
15 Ahimawaz, shi ne a Naftali (ya auri Basemat 'yar Solomon);
16 Ba'ana ɗan Hushai, shi ne a Asher da Bayelot;
17 Yehoshafat ɗan Faruwa, shi ne a Issakar;
18 Shimeyi ɗan Ela, shi ne a Benyamin;
19 Geber ɗan Uri, shi ne a Gileyad (ƙasar Sihon sarkin Amoriyawa da kuma Og sarkin Bashan). Shi ne kaɗai gwamna a bisa yankin.

### *Tanajin Solomon na kowace rana*

20 Mutanen Yahuda da na Isra'ila sun yi yawa sai ka ce yashi a bakin teku. Suka
ci, suka sha, suka kuma yi farin ciki. 21 Solomon kuwa ya yi mulki a bisa dukan
masarautai daga Kogi[*] zuwa ƙasar Filistiyawa, har zuwa iyakar Masar. Waɗannan
ƙasashe sun yi ta kawo haraji, suka kuma zama bayin Solomon dukan kwanakin
ransa.
22 Tanajin Solomon na kowace rana su ne, garwa talatin na garin abinci, 23 shanun
da aka yi kiwo a gida guda goma, shanu ashirin da suka ƙoshi daga kiwo, tumaki
da awaki ɗari; ban da ƙishimai, bareyi, batsiyoyi, da kaji masu ƙiba. 24 Gama ya
yi mulki a bisa dukan masarautai yamma da Kogi, daga Tifsa zuwa Gaza, aka kuwa
sami zaman lafiya a kowane gefe. 25 A kwanakin da Solomon yake raye, Yahuda da
Isra'ila, daga Dan zuwa Beyersheba, sun zauna lafiya, kowane mutum ya zauna a
ƙarƙashin itacen inabi da na ɓaurensa.
26 Solomon yana da rumfunan dawakai masu jan kekunan yaƙi, dubu huɗu,[†] da
kuma dawakai dubu goma sha biyu[‡]
27 Shugabannin yankuna, kowanne a watansa yakan yi tanajin abinci domin Sarki
Solomon da kuma duk wanda ya zo teburin sarki. Sun tabbatar ba a rasa kome ba.
28 Kowa a cikinsu, bisa ga lokacin da aka ba shi, yakan kai hatsin sha'ir da ciyawa
domin dawakan-kekunan yaƙi, da sauran dawakai a inda aka ajiye su.

### *Hikimar Solomon*

29 Allah ya ba Solomon hikima da hangen nesa mai girma, da kuma fāɗin fahimta
marar iyaka, kamar yashi a bakin teku. 30 Hikimar Solomon ta fi hikimar mutanen
Gabas, ta kuma fi dukan hikimar Masar girma. 31 Ya fi kowane mutum hikima, har
da Etan dangin Ezra ma. Yana da hikima fiye da Heman, Kalkol da Darda, 'ya'yan

* **4:21** Wato, Yuferites; haka ma a aya 24. † **4:26** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na Seftuwajin (dubi kuma 2Tar 9.25); Ibraniyanci na da arba'in ‡ **4:26** Ko kuwa masu hawa

Mahol maza. Sunansa ya bazu ko'ina a ƙasashen da suke kewaye. 32 Ya yi karin
magana dubu uku. Waƙoƙinsa kuwa sun kai dubu ɗaya da biyar. 33 Ya yi magana a
kan rayuwar itatuwa, daga al'ul na Lebanon zuwa hizzob da yake girma a bangaye.
Ya kuma yi koyarwa game da dabbobi, da tsuntsaye, da abubuwa masu rarrafe, da
kuma kifi. 34 Mutane suka yi ta zuwa daga ƙasashe dabam-dabam don su ji hikimar
Solomon. Sarakuna daga ko'ina a duniya, sun ji labarin hikimarsa, suka kuma aika
da mutane don su ji shi.

# 5

*Shirye-shirye don ginin haikali*
*(2 Tarihi 2.1-16)*

1 Sa'ad da Hiram sarkin Taya ya ji an shafe Solomon sarki yǎ gāji mahaifinsa
Dawuda, sai ya aika da jakadunsa zuwa wurin Solomon, gama shi da Dawuda abokai
ne sosai dukan kwanakinsa. 2 Solomon ya mayar da wannan saƙo ga Hiram ya ce,

3 "Ka san cewa saboda yaƙe-yaƙen da abokan gāba suka yi da mahaifina a
kowane gefe, ya sa bai iya gina haikali domin Sunan UBANGIJI Allahnsa ba, sai
da UBANGIJI ya sa abokan gābansa a ƙarƙashin ƙafafunsa. 4 Amma yanzu UBANGIJI
Allahna ya ba ni hutu a kowane gefe, babu kuma gāba ko masifa. 5 Ina niyya in
gina haikali domin Sunan UBANGIJI Allahna, yadda UBANGIJI ya faɗa wa mahaifina
Dawuda, sa'ad da ya ce, 'Ɗanka wanda zai gāje ka, shi zai gina haikali domin
Sunana.'

6 "Don haka, ka ba da umarni a yanka mini itatuwan al'ul na ƙasar Lebanon.
Ma'aikatana za su haɗa hannu da ma'aikatanka, ni kuwa zan biya ka albashin
ma'aikatanka kamar yadda ka faɗa. Gama ka san cewa babu wani a cikinmu da
ya iya yanka itacen katako kamar Sidoniyawa."

7 Da Hiram ya ji saƙon Solomon, sai ya ji daɗi ƙwarai, ya kuma ce, "Yabo ga UBANGIJI
a yau, gama ya ba wa Dawuda ɗa mai hikima yǎ yi mulki a bisa wannan al'umma
mai girma."

8 Sai Hiram ya aike wa Solomon da kalmomin nan,

"Na sami saƙon da ka aika mini, zan kuma yi duk abin da kake so ta wurin
tanada katakan al'ul da na fir. 9 Ma'aikatana za su gangara da su daga Lebanon
zuwa bakin teku. Zan sa a ɗaɗɗaura su su bi ruwan teku daga Lebanon zuwa
bakin Bahar Rum da za ka nuna mini. A can zan kunce maka su, sa'an nan ka
kwashe. Kai kuma za ka biya bukatata ta wurin tanadin abinci wa gidana."

10 A haka Hiram ya ci gaba da aika wa Solomon al'ul da kuma fir da yake bukata.
11 Solomon kuma ya ba wa Hiram mudu gari dubu ashirin na alkama a matsayin
abinci domin gidansa, ya ƙara da garwa dubu ashirin na tataccen man zaitun.
Solomon ya ci gaba da yin haka ga Hiram, shekara-shekara. 12 UBANGIJI ya ba wa
Solomon hikima, kamar yadda ya yi masa alkawari. Dangantakar zaman lafiya ta
kasance tsakanin Hiram da Solomon, su biyun suka yi yarjejjeniya.

13 Sarki Solomon ya ɗebi ma'aikata daga dukan Isra'ila, su dubu talatin. 14 Ya
riƙa aika su dubu goma-goma zuwa Lebanon kowane wata, saboda su yi wata ɗaya
a Lebanon, watanni biyu kuma a gida. Adoniram ne ya lura da aikin gandun.
15 Solomon ya kasance da 'yan ɗauko guda dubu saba'in da masu yankan duwatsu
guda dubu tamanin a cikin tuddai, 16 ya kuma kasance da shugabanni dubu uku da
ɗari uku waɗanda suke lura da aikin, su ne kuma suke bi da ma'aikatan. 17 Bisa
ga umarnin sarki sai suka cire manyan duwatsu masu kyau don a tanada tushen
duwatsun da aka gyara domin haikalin daga wurin haƙar duwatsun. 18 Gwanayen

Solomon da na Hiram da kuma mutanen Gebal[*], su suka yanka, suka kuma shirya
katako da dutse don ginin haikali.

# 6

### *Solomon ya gina haikali*

1 A shekara ta ɗari huɗu da tamani bayan fitowar Isra'ilawa daga Masar, a shekara
ta huɗu ta mulkin Solomon a bisa Isra'ila, a watan Zif, wata na biyu, Solomon ya fara
gina haikalin UBANGIJI.
2 Haikalin da Sarki Solomon ya gina wa UBANGIJI, tsawonsa kamu sittin, fāɗinsa
kamu ashirin, tsayinsa kuma kamu talatin ne. 3 Shirayin da yake a gaban ainihin
zauren haikalin, ya ƙara faɗin haikalin da kamu ashirin, ya kuma nausa daga gaban
haikalin kamu goma. 4 Ya yi tagogin da suka fi fāɗi daga ciki fiye da waje a haikalin.
5 A jikin bangayen babban zaure da kuma cikin wuri mai tsarki, ya gina ɗakuna
kewaye da ginin, inda akwai ɗakuna a gefe. 6 Fāɗin ɗakunan ƙasa, kamu biyar ne,
fāɗin ɗakunan tsakiya, kamu shida ne, fāɗin ɗakunan hawa na uku kuwa, kamu
bakwai ne. Ya yi bangaye kewaye a waje da haikalin don kada a sa wani abu a
bangayen haikali.
7 A yin ginin haikalin, duwatsun da aka fafe ne kaɗai daga wurin fafe duwatsu aka
yi amfani da su, ba a ji karar guduma ko gizago, ko wani abin da aka yi da ƙarfe a
wurin ginin haikali yayinda ake gina shi ba.
8 Kofar zuwa ɗakunan ƙasa tana gefen kudu na haikalin; akwai matakai da suka
bi zuwa hawa na tsakiya, daga can kuma matakan sun wuce zuwa hawa na uku. 9 A
haka ya gina haikalin ya kuma gama shi, ya jinƙe shi da manyan katakai da kuma
katakan al'ul. 10 Ya kuma gina ɗakunan gefe duka a gefen haikalin. Tsayin kowanne,
kamu biyar ne, aka haɗa su da haikalin da manyan katakan al'ul.
11 Sai maganar UBANGIJI ta zo wa Solomon ta ce, 12 "Game da wannan haikalin
da kake ginawa, in ka bi ƙa'idodina, ka cika farillaina, ka kiyaye dukan umarnaina,
ka kuma yi biyayya da su, zan cika alkawarin da na yi wa mahaifinka Dawuda ta
wurinka. 13 Zan kuma zauna a cikin Isra'ilawa, ba kuwa zan taɓa rabuwa da su ba."
14 Saboda haka Solomon ya gina haikalin ya kuma gama shi.

*(2 Tarihi 3.8-14)*

15 Ya rufe bangon ciki da katakan itacen al'ul tun daga ƙasa har zuwa sama, ya
kuma rufe daɓen da katakan itacen fir. 16 Ya gina Wuri Mafi Tsarki na can ciki, ya
gina shi a can ƙuryar haikalin. Tsayinsa kamu ashirin ne, an manne masa katakan
itacen al'ul tun daga ƙasa har zuwa sama. 17 Tsawon babban zaure a gaban wannan
ɗaki, kamu arba'in ne. 18 An yi wa katakan itacen al'ul na cikin haikalin zāne mai
fasalin gora da na buɗaɗɗun furanni. An rufe bangon ciki duka da itacen al'ul, har
ba a ganin duwatsun ginin.
19 Ya shirya wuri mai tsarki na ciki can cikin haikali don yǎ sa akwatin alkawarin
UBANGIJI a can. 20 Tsawon wuri mai tsarki na ciki kamu ashirin, fāɗin kamu ashirin,
tsayin kuma kamu ashirin. Ya dalaye cikin da zinariya zalla, ya kuma dalaye bagade
al'ul ɗin. 21 Solomon ya rufe cikin haikalin da zinariya zalla, ya kuma gifta sarƙoƙin
zinariya a gaban wuri mai tsarki na ciki, wanda aka dalaye da zinariya. 22 Haka ya
dalaye dukan cikin da zinariya. Ya kuma dalaye bagade na cikin wuri mai tsarki da
zinariya.
23 A wuri mai tsarki na can ciki, ya yi kerubobi biyu na itacen zaitun, kowanne
mai tsayi kamu goma. 24 Fiffike ɗaya na kerub na fari tsawonsa kamu biyar ne,
ɗayan fiffike kuma kamu biyar, kamu goma daga ƙarshen fiffike zuwa ƙarshen fiffike.
25 Kerub na biyun shi ma kamu goma ne, gama kerubobi biyun sun yi kama da juna a

* **5:18** Wato, Baibilos.

girma da kuma siffa. 26 Tsayin kowane kerub kamu goma ne. 27 Ya ajiye kerubobin a
ɗaki na can cikin haikalin, da fikafikansu a buɗe. Fiffiken kerub ɗaya ya taɓa bango
guda, yayinda fiffiken ɗayan ya taɓa ɗayan bangon, kuma fikafikansu sun taɓa juna
a tsakiyar ɗakin. 28 Ya dalaye kerubobin da zinariya.
29 A bangaye kewaye da haikali, a ɗakuna ciki da waje, ya zāzzāna kerubobi,
itatuwan dabino, da furanni buɗaɗɗu. 30 Ya kuma rufe ƙasan ɗakuna ciki da wajen
haikali da zinariya.
31 Don ƙofar shiga wuri mai tsarki na ciki kuwa, ya yi ƙofofin katakon zaitun
da madogarai masu gefe biyar. 32 A kan ƙofofin katakan zaitun kuwa ya zāzzāna
kerubobi, itatuwa dabino, da furanni buɗaɗɗu, ya kuma dalaye kerubobin, da kuma
itatuwan dabinon da zinariya. 33 Haka ma ya yi madogarai masu gefe huɗu na
katakon zaitun don ƙofar shiga zuwa babban zaure. 34 Ya yi ƙofofi biyu na itacen
fir, kowanne yana da shafi biyu da suke juyewa a maɗaurai. 35 Ya zāzzāna kerubobi,
itatuwan dabino, da kuma furanni buɗaɗɗu a kansu, ya kuma dalaye su da zinariyar
da aka buga daidai a kan sassaƙa.
36 Ya kuma gina filin ciki da sassaƙaƙƙun duwatsu, jeri uku, da jeri ɗaya na katakan
itacen al'ul.
37 An kafa tushen haikalin Ubangiji a shekara ta huɗu, a watan Zif. 38 A shekara
ta goma sha ɗaya, a watan Bul, wata na takwas ke nan, aka gama haikalin daidai
yadda aka tsara shi bisa ga fasalinsa. Solomon ya ɗauki shekara bakwai yana ginin
haikalin.

# 7

*Solomon ya gina fadarsa*

1 Ya ɗauki Solomon shekaru goma sha uku kafin yă gama gina fadarsa. 2 Ya gina
fadarsa mai suna Kurmin Lebanon, tsawonsa kamu ɗari, fāɗinsa kamu hamsin,
tsayinsa kuma kamu talatin, a bisa jeri huɗu na ginshiƙan itacen al'ul, aka shimfiɗa
katakan itacen al'ul a bisa ginshiƙan. 3 Aka yi rufin da al'ul bisa ginshiƙan da suke
bisa ginshiƙai arba'in da biyar, goma sha biya a kowane jeri. 4 Aka kuma yi tagogi
masu sandunan ƙarfe, jeri uku, kowace taga tana ɗaura da 'yar'uwarta, har jeri uku.
5 Dukan ƙofofin da madogaransu murabba'i ne, taga kuma tana ɗaura da 'yar'uwarta
har jeri uku.
6 Ya yi babban zaure mai ginshiƙai, tsawonsa kamu hamsin, fāɗinsa kuwa kamu
talatin. A gabansa kuwa akwai shirayi, kuma a gaban wannan shirayi akwai ginshiƙai
da kuma rufin da yake a shimfiɗe.
7 Ya kuma gina shirayi ta sarauta, da ya kira Zauren Adalci, inda zai riƙa yin shari'a,
ya kuma rufe dukan daɓensa da itacen al'ul daga ƙasa har sama. 8 A fadar da zai
zauna kuwa, wadda aka gina a can baya, ya yi ta da irin fasali guda. Solomon ya
kuma yi wata fada kamar wannan zaure domin 'yar Fir'auna, wadda ya auro.
9 Dukan waɗannan gine-gine, daga waje zuwa babban fili, da kuma daga tushen
zuwa rufin, an yi su da duwatsun da aka yanka, aka kuma gyara da zarto a
fuskokinsu na ciki da waje. 10 Aka kafa tushen da manyan duwatsu masu kyau, tsayin
waɗansunsu ya kai kamu goma, waɗansu kuma kamu takwas. 11 A can bisa akwai
duwatsu masu tsada da aka yayyanka bisa ga ma'auni, da kuma ginshiƙan al'ul. 12 An
kewaye babban filin da katanga da jerin uku-uku na duwatsun da aka gyara, da kuma
jeri guda na gyararren al'ul, kamar yadda aka yi na filin cikin haikalin Ubangiji da
shirayinsa.

*Kayan haikali*
*(2 Tarihi 3.15-17; 4.1-10)*

13 Sarki Solomon ya aika zuwa Taya aka kuma kawo Huram, 14 wanda mahaifiyarsa
gwauruwa ce daga kabilar Naftali, wanda kuma mahaifinsa mutumin Taya ne, shi
Huram, gwani ne a aikin tagulla. Huram gwani ne sosai kuma ya saba da yin kowane
irin aikin tagulla. Sai ya zo wurin Sarki Solomon ya kuma yi dukan aikin da aka sa
shi.
15 Ya yi ginshiƙan tagulla, kowanne tsayinsa kamu goma sha takwas, ya kuma yi
guru mai kamu goma sha biyu, kewaye da shi. 16 Ya yi dajiyoyi biyu na zubin tagulla
don yǎ sa a bisa ginshiƙai; kowace dajiya tsayinta kamu biyar ne. 17 Aka yi yanar
tuƙaƙƙun sarƙoƙi aka ɗaura dajiyoyin a bisa ginshiƙai guda bakwai don kowace
dajiya. 18 Ya yi rumman jeri biyu kewaye da kowace yanar don yǎ yi adon dajiyoyin
a bisa ginshiƙan. Haka kuma ya yi wa ɗaya dajiyar. 19 Dajiyoyin da suke a bisa
ginshiƙan a shirayi suna da fasalin furen bi-rana, tsayinsu kamu huɗu-huɗu ne. 20 A
inda kan ginshiƙin ya buɗu kamar kwano, sama da zāne-zānen sarƙar, an yi zāne-
zānen rumman wajen ɗari biyu, layi-layi kewaye da kawunan ginshiƙan nan. 21 Ya
ta da ginshiƙai a shirayin haikali. Ya ba wa ginshiƙi na wajen kudu sunan Yakin,*
na wajen arewa kuma ya kira Bowaz.† 22 Dajiyoyin da suke a bisa suna da fasalin
bi-rana ne. Ta haka aka gama aiki a kan ginshiƙan.
23 Sai Huram ya yi wani ƙaton kwano na ƙarfen tagulla, da ya kira Teku. Zurfin
kwanon nan kamu bakwai da rabi, fāɗinsa kamu goma sha biyar, da'irarsa kuma
kamu talatin ne. 24 A kewayen bakin ƙaton kwanon akwai layi biyu na siffofin goran
ƙarfen tagulla, akwai gora shida cikin kowane ƙafa. An yi zubinsu haɗe da kwanon
nan da kira Teku.
25 Kwanon ya tsaya a kan siffofin bijimai goma sha biyu, uku suna fuskantar arewa,
uku suna fuskantar yamma, uku suna fuskantar kudu, sa'an nan uku suna fuskantar
gabas. Kwanon da ya kira Teku ya zauna a kansu, gindin siffofin bijimai goma sha
biyun nan suna wajen tsakiya. 26 Kaurin kwanon ya kai tafin hannu, kuma da'iransa
ya yi kamar da'iran kwaf, kamar bi-ranar da ta buɗe. Wannan kwanon da aka kira
Teku yakan ci garwa dubu biyu.
27 Ya kuma yi dakalai guda goma na tagulla da ake iya matsar da su; kowane
tsawonsa kamu huɗu ne, fāɗinsa kamu huɗu, tsayinsa kuma kamu uku. 28 Ga yadda
aka yi dakalan, dakalan suna da ɓangarori haɗe da mahaɗai. 29 A bisa sassan
tsakanin mahaɗan, akwai siffofin zakoki, bijimai da kuma kerubobi, suna a kan
mahaɗan su ma. A sama da kuma ƙasan siffofin zakokin da na bijiman kuwa akwai
hotunan furanni. 30 Kowane dakali yana da ƙafa huɗu na tagulla kamar na keken
yaƙi, da sandunan tagulla don sa kwanon nan da aka kira Teku. A kusurwoyin akwai
abubuwan zubi don riƙe kwanon. An zāna furanni a kowane gefensu. 31 A dakalin
daga ciki, akwai bakin da yake da'ira, mai zurfi kamun guda. Bakin da'irar ne, yana
da zāne-zānensa da ya kai kamu ɗaya da rabi. Kusa da bakin akwai zāne-zāne.
Sassan dakalin murabba'i ne, ba da'ira ba ne. 32 Kafafu huɗun suna a ƙarƙashin
ɓangarorin, aka kuma haɗa gindin ƙafafun keken da dakalin. Tsayin kowace ƙafa
kamu ɗaya da rabi ne. 33 An yi ƙafafun kamar ƙafafun keken yaƙi ne; gindin, da'irar,
gyaffan da kuma cibiyar duk an yi su da ƙarfe ne.
34 Kowane dakali yana da hannuwa huɗu, ɗaya a kowane gefe, da yake nausawa
daga dakalin. 35 A bisa dakalin akwai da'irar da ta yi kamar gammo mai zurfi kamar
rabin kamu‡. Abubuwan da suke riƙewa da kuma sassan, an haɗa su da bisa dakalin.
36 Ya zāna siffofin kerubobi, zakoki da itatuwan dabino a saman abubuwan riƙewa
da kuma a kan ɓangarorin, a kowane abin da ya ga akwai ɗan fili, ya zāna furanni.

* **7:21** Yakin mai yiwuwa yana nufin ya kafa. † **7:21** Bowaz mai yiwuwa yana nufin a cikinsa akwai ƙarfi.
‡ **7:35** Wato, kamar inci 9 ko kuma kamar sentimita 23

37 Haka ya yi dakalai goma. Duk an yi zubinsu iri ɗaya ne, girmansu da fasalinsu
kuma iri ɗaya.
38 Sa'an nan ya yi kwanoni goma na tagulla, kowane yana cin garwa arba'in, kuma
kamu huɗu daga wannan zuwa wancan, kowane dakali yana da daro ɗaya. 39 Ya sa
dakalai biyar a gefen kudu na haikali, biyar kuma a arewa. Ya sa kwanon a gefen
kudu, a gefen kudu maso gabas na haikalin. 40 Ya kuma yi kwanoni da manyan cokula
da kuma kwanonin yayyafawa.

*(2 Tarihi 4.11–5.1)*

Ta haka Huram ya gama dukan aikin da ya yi wa Sarki Solomon a haikalin Ubangiji.

41 Ya yi ginshiƙai biyun;
dajiyoyi biyu masu fasalin kwano a kan ginshiƙan;
ya yi yanar kashi biyu wa dajiyoyi masu fasalin kwano guda biyu a kan ginshiƙai;
42 ya yi rumman guda ɗari huɗu na sashi yanar biyun (jeri biyu na rumman don kowace yanar, yana adon dajiyoyi masu fasalin kwano a kan ginshiƙai);
43 ya yi dakalai goma da kwanoninsu goma;
44 ya yi kwanon da ya kira Teku, da bijimai goma sha biyu a ƙarƙashinsa;
45 ya yi tukwane, manyan cokula da kwanonin yayyafawa.

Dukan waɗannan abubuwan da Huram ya yi wa Sarki Solomon saboda haikalin
Ubangiji, an dalaye su da tagulla. 46 Sarki ya sa aka yi zubi a abin yin tubalin laka
a filin Urdun, tsakanin Sukkot da Zaretan. 47 Solomon ya bar dukan waɗannan
abubuwa ba tare da an auna su ba, domin sun yi yawa sosai; ba a san nauyin tagullar
ba.
48 Solomon ya kuma yi dukan kayayyakin da suke cikin haikalin Ubangiji.

Ya yi bagaden zinariya;
teburin zinariya, inda ake ajiye burodin Kasancewa;
49 ya yi alkukai na zinariya zalla (Biyar a dama, biyar kuma a hagu, a gaban wuri mai tsarki na can cikin);
ya yi zāne-zānen furannin zinariya da fitilu da kuma arautaki;
50 ya yi kwanonin zinariya zalla, hantsuka, kwanonin yayyafawa, kwanoni, da kuma farantan wuta;
ya yi wurin ajiye fitila na zinariya domin ƙofofi na ɗakin can ciki-ciki, da na ƙofofin Wuri Mafi Tsarki, da kuma domin ƙofofin babban zauren haikali.

51 Sa'ad da aka gama aikin da Sarki Solomon sa a yi domin haikalin Ubangiji, sai ya
kawo kayayyakin da mahaifinsa Dawuda ya keɓe, azurfa da zinariya da kayayyaki,
ya sa su a ma'ajin haikalin Ubangiji.

# 8

## *An kawo akwatin alkawari a haikali*

*(2 Tarihi 5.2–6.2)*

1 Sai Sarki Solomon ya tattara dattawan Urushalima a gabansa, da dukan
shugabannin kabilu, da shugabannin iyalan Isra'ilawa, domin su kawo akwatin
alkawarin Ubangiji daga Sihiyona, Birnin Dawuda. 2 Dukan mutanen Isra'ila suka
tattaru a gaban Sarki Solomon a lokacin biki, a watan Etanim, wato, wata na bakwai.
3 Sa'ad da dukan dattawan Isra'ila suka iso, sai firistoci suka ɗauki akwatin
alkawarin, 4 suka haura da akwatin alkawarin Ubangiji da kuma Tentin Sujada, da
dukan kayayyaki masu tsarkin da suke cikinsa. Firistoci da Lawiyawa suka ɗauko
su, 5 sai Sarki Solomon da dukan taron Isra'ila da suka tattaru kewaye da shi a gaban

akwatin alkawari, suka yi ta miƙa hadayar tumaki da bijimai masu yawa da ba a iya lissaftawa, ko ƙirgawa.

6 Sa'an nan firistoci suka kawo akwatin alkawarin UBANGIJI inda aka shirya masa,
can ciki cikin haikali, a Wuri Mafi Tsarki, aka kuma sa shi a ƙarƙashin fikafikan
kerubobin. 7 Kerubobin sun buɗe fikafikansu a bisa wurin da akwatin alkawarin
yake, suka inuwartar da akwatin alkawarin da sandunan ɗaukansa. 8 Waɗannan
sandunan sun yi tsawo har ana iya ganin bakinsu daga Wuri Mai Tsarki a gaban
wuri mai tsarki na can ciki, amma ba a iya ganinsu daga waje na Wuri Mai Tsarki
ba. Suna nan kuwa a can har wa yau. 9 Ba kome a cikin akwatin alkawarin, sai dai
alluna na dutse guda biyu waɗanda Musa ya ajiye a ciki tun a Horeb, inda UBANGIJI
ya yi alkawari da Isra'ilawa bayan sun fito Masar.

10 Sa'ad da firistoci suka janye daga Wuri Mai Tsarki, sai girgije ya cika haikalin
UBANGIJI. 11 Firistocin kuwa ba su iya yin hidimarsu ba saboda girgijen, gama
ɗaukakar UBANGIJI ta cika haikalinsa.

12 Sai Solomon ya ce, "UBANGIJI ya ce zai zauna a gizagizai masu duhu; 13 ga shi na
gina haikali mai daraja dominka, inda za ka zauna har abada."

*(2 Tarihi 6.3-11)*

14 Yayinda dukan taron Isra'ila suke tsattsaye a can, sai sarki ya juya ya albarkace
su. 15 Sa'an nan ya ce,

"Ku yabi UBANGIJI, Allah na Isra'ila, wanda da hannunsa ya cika abin da ya yi
alkawari da bakinsa ga mahaifina Dawuda. Gama ya ce, 16 'Tun ran da na fitar
da mutanena Isra'ila daga Masar, ban zaɓi wani birni a cikin wata kabilar Isra'ila
a gina haikali domin Sunana yă kasance a can ba, amma na zaɓi Dawuda yă yi
mulkin mutanena Isra'ila.'

17 "Mahaifina Dawuda ya yi niyya a cikin zuciyarsa yă gina haikali saboda Sunan
UBANGIJI, Allah na Isra'ila. 18 Amma UBANGIJI ya ce wa mahaifina Dawuda, 'Saboda
yana a zuciyarka ka gina haikali domin Sunana, ka yi daidai da ka yi niyyar wannan
a zuciyarka. 19 Duk da haka, ba kai ba ne za ka gina haikali, amma ɗanka, wanda
yake namanka da jininka, shi ne wanda zai gina haikali domin Sunana.'

20 "UBANGIJI ya kiyaye alkawarin da ya yi. Na gāje Dawuda mahaifina, yanzu
kuma ga shi na zauna a kujerar sarautar Isra'ila, kamar dai yadda UBANGIJI ya
yi alkawari, na kuma gina haikali domin Sunan UBANGIJI, Allah na Isra'ila. 21 Na
tanada wuri saboda akwatin alkawari, akwatin da ya ƙunshi alkawarin da UBANGIJI
ya yi da kakanninmu sa'ad da ya fitar da su daga Masar."

## *Addu'ar Solomon ta miƙawa*
*(2 Tarihi 6.12-42)*

22 Sai Solomon ya tsaya a gaban bagaden UBANGIJI, a gaban dukan taron Isra'ila, ya
ɗaga hannuwansa sama, 23 ya ce,

"Ya UBANGIJI, Allah na Isra'ila, babu Allah kamar ka a sama can bisa, ko a ƙasa
can ƙarƙashi, kai da kake kiyaye alkawarinka na ƙauna ga bayinka waɗanda suke
cin gaba a hanyarka da dukan zuciyarsu. 24 Ka kiyaye alkawarinka da ka yi wa
bawanka Dawuda mahaifina. Da bakinka ka yi alkawari, da hannunka kuma ka
cika shi, yadda yake a yau.

25 "Yanzu, ya UBANGIJI, Allah na Isra'ila, bari ka cika wa bawanka Dawuda
mahaifina alkawaran da ka yi masa sa'ad da ka ce, 'Ba za ka taɓa rasa wani da
zai zauna a gabana a kan kujerar sarautar Isra'ila ba, in kawai 'ya'yanka maza
sun yi hankali cikin dukan abubuwan da suke yi, don su yi tafiya a gabana kamar
yadda ka yi.' 26 Yanzu fa, ya Allah na Isra'ila, bari maganarka da ka yi wa bawanka
Dawuda mahaifina tă cika.

27 “Amma anya, Allah, za ka zauna a duniya? Sammai, har ma da saman sammai
ba za tă iya riƙe ka ba, balle wannan haikalin da na gina! 28 Duk da haka ka ji
addu’ar bawanka da kuma roƙonsa don jinƙai, ya Ubangiji Allahna. Ka ji kuka
da addu’ar da bawanka yake yi a gabanka a wannan rana. 29 Bari idanunka su
buɗe, su fuskanci wannan haikali dare da rana, wannan wurin da ka ce, ‘Sunana
zai kasance a can,’ saboda ka ji addu’ar bawanka in yana fuskantar wannan wuri.
30 Ka ji roƙon bawanka da kuma na mutanenka Isra’ila sa’ad da suka yi addu’a,
suka fuskanci wannan wuri. Ka ji daga sama, mazauninka, kuma sa’ad da ka ji, ka
gafarta.

31 “Sa’ad da mutum ya yi abin da ba daidai ba ga maƙwabcinsa, an kuma bukace
shi yă yi rantsuwa, sai ya zo ya rantse a gaban bagade a cikin haikalin nan, 32 sai
ka ji daga sama, ka kuma yi wani abu. Ka shari’anta tsakanin bayinka, ka hukunta
mai laifi, ka mai da laifinsa a kansa, mai gaskiya kuma ka nuna shi marar laifi ne
bisa ga gaskiyarsa.

33 “Sa’ad da abokan gāba suka ci mutanenka Isra’ila a yaƙi saboda sun yi maka
zunubi, sa’ad da kuma suka dawo gare ka don su furta sunanka, suna addu’a suna
roƙo gare ka a wannan haikali, 34 ka ji daga sama, ka gafarta zunubin mutanenka,
ka kuma dawo da su ƙasar da ka ba wa kakanninsu.

35 “Sa’ad da sammai sun kulle, babu kuma ruwan sama domin mutane sun yi
maka zunubi, sa’ad da suka yi addu’a suna fuskantar wannan wuri, suka kuma
furta sunanka, suka juye daga zunubinsu domin ka hore su, 36 ka ji daga sama, ka
kuma gafarta zunubin bayinka, mutanenka Isra’ila. Ka koya musu hanyar da ta
dace ta rayuwa, ka kuma aika da ruwan sama a ƙasar da ka ba wa mutanenka
gādo.

37 “Sa’ad da yunwa ko annoba ta fāɗo a ƙasar, ko burtuntuna, ko fumfuna, ko
fāri, ko tsutsa, ko kuwa abokan gāba sun yi musu kwanto, a wani daga cikin
biranensu, duk wata cuta, ko ciwon da ya zo, 38 in suka yi addu’a ko roƙo ta wurin
wani daga cikin mutanenka Isra’ila, kowa ya san wahalar zuciyarsa, ya kuma buɗe
hannuwansa yana fuskantar wannan haikali, 39 sai ka ji daga sama, mazauninka.
Ka gafarta, ka kuma yi wani abu. Ka yi da kowane mutum bisa ga dukan abin da ya
yi, tun da yake ka san zuciyarsa (gama kai kaɗai ka san zukatan dukan mutane),
40 saboda su ji tsoronka a kowane lokacin da suke zaune a ƙasar da ka ba wa
kakanninmu.

41 “Game da baƙo kuwa wanda shi ba na mutanenka Isra’ila ba, amma ya zo daga
ƙasa mai nisa saboda sunanka, 42 gama mutane za su ji game da girman sunanka,
da ƙarfin hannunka, da kuma hannunka mai iko, sa’ad da ya zo, ya yi addu’a yana
fuskantar wannan haikali, 43 ka ji daga sama, mazauninka, ka kuma yi dukan abin
da baƙon ya tambaye ka, saboda dukan mutanen duniya su san sunanka, su kuma ji
tsoronka, kamar yadda mutanenka Isra’ila suke yi, bari kuma su san cewa wannan
gidan da na gina, ya amsa Sunanka.

44 “Sa’ad da mutanenka suka tafi yaƙi da abokan gābansu, a duk inda ka aike
su, sa’ad da kuma suka yi addu’a ga Ubangiji suna fuskantar birnin da ka zaɓa,
da kuma haikalin da na gina domin Sunanka, 45 ka ji addu’arsu da roƙonsu daga
sama, ka kuma biya musu bukatansu.

46 “Sa’ad da suka yi maka zunubi, gama babu wanda ba ya zunubi, ka kuwa yi
fushi da su, ka kuma ba da su ga abokin gāba, wanda ya kwashe su kamammu
zuwa ƙasarsa, nesa ko kusa; 47 in suka canja zuciyarsu a ƙasar da aka riƙe su
kamammu, suka tuba, suka kuma roƙe ka a ƙasar waɗanda suka ci su da yaƙi, suka
ce, ‘Mun yi zunubi, mun yi abin da ba daidai ba, mun yi mugunta’; 48 in sun juye
gare ka da dukan zuciyarsu, da dukan ransu a ƙasar abokan gābansu waɗanda

suka kwashe kamammu, suka yi addu'a gare ka, suka fuskanci wajen ƙasar da ka
ba wa kakanninsu, waje birnin da ka zaɓa, da kuma haikalin da na gina domin
Sunanka; 49 sai ka ji daga sama, mazauninka, ka ji addu'a da roƙonsu, ka kuma
biya musu bukatansu. 50 Ka gafarta wa mutanenka, waɗanda suka yi maka zunubi;
ka gafarta dukan laifofin da suka yi maka, ka kuma sa waɗanda suka ci su a yaƙi
su ji tausayinsu. 51 Gama su mutanenka ne, abin gādonka, waɗanda ka fitar daga
Masar, daga tanderu mai narken ƙarfe.

52 "Bari idanunka su buɗe ga roƙon bawanka, ga roƙon mutanenka Isra'ila, bari
kuma ka saurare su sa'ad da suka yi kuka gare ka. 53 Gama ka ware su daga dukan
al'umman duniya su zama abin gādonka, kamar yadda aka furta ta wurin bawanka
Musa sa'ad da kai, ya Ubangiji Mai Iko Duka ka fitar da kakanninmu daga Masar."

54 Da Solomon ya gama dukan waɗannan addu'o'i da roƙe-roƙe ga Ubangiji, sai ya
tashi daga gaban bagaden Ubangiji, inda ya durƙusa da hannuwansa a buɗe waje
sama. 55 Ya tashi ya kuma albarkaci dukan taron Isra'ila da babbar murya, yana
cewa,

56 "Yabo ya tabbata ga Ubangiji, wanda ya ba wa mutanensa hutu kamar dai
yadda ya yi alkawari. Babu magana guda da ta kāsa cika cikin dukan alkawaransa
masu kyau da ya yi ta wurin bawansa Musa. 57 Bari Ubangiji Allah yǎ kasance
tare da mu kamar yadda ya kasance da kakanninmu; kada yǎ taɓa rabu da mu, ko
yǎ yashe mu. 58 Bari yǎ juye zukatanmu gare shi, don mu yi tafiya a cikin dukan
hanyoyinsa, mu kuma kiyaye umarnansa, ƙa'idodinsa, da kuma farillan da ya ba
wa kakanninmu. 59 Bari kuma waɗannan kalmomina, waɗanda na yi addu'a a
gaban Ubangiji, su yi kusa da Ubangiji Allahnmu, dare da rana, don yǎ biya bukatan
bawansa da na mutanensa Isra'ila, bisa ga bukatan kowa, 60 saboda dukan mutanen
duniya su san cewa Ubangiji, shi ne Allah, babu kuma wani. 61 Amma dole ku miƙa
zukatanku ga Ubangiji Allahnmu, don ku rayu, ta wurin bin ƙa'idodinsa, ku kuma
yi biyayya da umarnansa, kamar yadda kuke yi a wannan lokaci."

### *Keɓewar haikali*
### *(2 Tarihi 7.4-10)*

62 Sai sarki da dukan Isra'ila, suka miƙa hadayu a gaban Ubangiji. 63 Solomon ya
miƙa hadaya ta salama ga Ubangiji, shanu dubu ashirin da biyu, tumaki da awaki
dubu ɗari da dubu ashirin. Ta haka sarki da dukan Isra'ilawa suka keɓe haikalin
Ubangiji.

64 A wannan rana sarki ya tsarkake sashe na tsakiyar fili a gaban haikalin Ubangiji,
a can kuma ya miƙa hadaya ta ƙonawa, hadaya ta gari, da kitsen hadaya ta salama,
gama bagaden tagulla a gaban Ubangiji ya yi ƙanƙanta sosai da za a miƙa hadayun
ƙonawa, hadayun hatsi, da kuma kitsen hadayun salama.

65 Ta haka Solomon da dukan Isra'ila, wato, babban taro, suka yi bikin a lokacin.
Mutane suka zo, tun daga Lebo Hamat har zuwa Rafin Masar. Suka yi biki a gaban
Ubangiji Allahnmu, kwana bakwai. Suka kuma ƙara kwana bakwai, kwanaki goma
sha huɗu gaba ɗaya. 66 A rana ta biye sai ya sallame mutane. Suka sa wa sarki
albarka, sa'an nan suka watse zuwa gida, da farin ciki, da murna a zukatansu
saboda kyawawan abubuwan da Ubangiji ya yi domin bawansa Dawuda, da kuma
mutanensa Isra'ila.

## 9

### *Ubangiji ya bayyana ga Solomon*
### *(2 Tarihi 7.11-22)*

1 Sa'ad da Solomon ya gama ginin haikalin UBANGIJI da kuma fadan sarki, ya kuma
yi dukan abin da yake so yă yi, 2 sai UBANGIJI ya bayyana gare shi sau na biyu, kamar
yadda ya bayyana masa a Gibeyon. 3 UBANGIJI ya ce masa,

"Na ji addu'arka da kuma roƙon da ka yi a gabana; na tsarkake wannan haikali wanda ka gina, ta wurinsa Sunana zai kasance a can har abada. Idanuna da zuciyata kullum za su kasance a can.

4 "Kai kuwa, in ka yi tafiya a gabana da mutunci a zuci da kuma gaskiya, kamar
yadda Dawuda mahaifinka ya yi, ka yi dukan abin da na umarta, ka kuma yi
biyayya da ƙa'idodina da kuma dokokina, 5 zan kafa kujerar sarautarka a bisa
Isra'ila har abada, kamar yadda na alkawarta wa Dawuda mahaifinka sa'ad da na
ce, 'Ba za ka taɓa rasa wani a kan kujerar sarautar Isra'ila ba.'

6 "Amma in kai, ko 'ya'yanka maza, suka juye daga gare ni, ba ku kuma kiyaye
umarnai da ƙa'idodin da na ba ku ba, kuka yi gaba, kuka bauta wa waɗansu alloli,
kuka kuma yi musu sujada, 7 sai in yanke mutanen Isra'ila daga ƙasar da na ba
su, in kuma ƙi wannan haikalin da na tsarkake domin Sunana. Isra'ila kuwa za tă
zama abin gori da abin dariya a cikin dukan mutane. 8 Wannan haikali zai zama
tarin juji. Duk wanda ya wuce ta hanyan nan kuwa zai ji tausayi, yă kuma yi
tsaki yana cewa, 'Me ya sa UBANGIJI ya yi haka ga wannan ƙasa da kuma wannan
haikali?' 9 Mutane za su amsa su ce, 'Saboda sun yashe UBANGIJI Allahnsu, wanda
ya fitar da su daga Masar, suka rungumi waɗansu alloli, suna yin musu sujada,
suna bauta musu ne, ya sa UBANGIJI ya kawo dukan masifan nan a kansu.' "

### *Waɗansu ayyukan Solomon*
### *(2 Tarihi 8.1-18)*

10 A ƙarshen shekaru ashirin da Solomon ya ɗauka yana gina haikalin UBANGIJI da
fadan sarki, 11 sai Sarki Solomon ya ba wa Hiram sarkin Taya garuruwa ashirin a
yankin Galili, gama Hiram ya tanada masa da dukan katakai al'ul da na fir, da kuma
zinariyar da ya bukaci domin aiki. 12 Amma sa'ad da Hiram ya zo daga Taya don
yă ga garuruwan da Solomon ya ba shi, sai bai ji daɗi ba. 13 Sai ya ce, "Wanda irin
garuruwa ke nan ka ba ni, ɗan'uwana?" Saboda haka ya kira su Kasar Kabul[*], sunan
da suke da shi har wa yau. 14 Hiram kuwa ya aika wa sarki talenti 120[†] na zinariya.

15 Ga lissafin ma'aikatan gandun da Sarki Solomon ya ɗauka don ginin haikalin
UBANGIJI, da fadarsa, da madogaran gini, da katangar Urushalima, da kuma Hazor
Megiddo da Gezer. 16 (Fir'auna sarkin Masar ya kai wa Gezer hari, ya kuma ci ta
da yaƙi. Ya sa mata wuta, ya kashe Kan'aniyawanta mazaunan wurin, ya kuma ba
da ita a matsayin kyautar aure ga 'yarsa, matar Solomon. 17 Solomon kuwa ya sāke
gina Gezer.) Ya gina Bet-Horon ta Kwari, 18 da Ba'alat, da Tadmor a hamada, na
cikin ƙasarsa. 19 Haka kuma ya gina dukan biranen ajiyarsa, da garuruwa domin
kekunan yaƙinsa, da garuruwa domin dawakansa. Ya gina duk abin da ya so yă
ginawa a Urushalima, da Lebanon, da kuma ko'ina a dukan yankin da ya yi mulki.

20 Dukan Amoriyawa, da Hittiyawa, da Ferizziyawa, da Hiwiyawa da Yebusiyawan
da suka ragu a ƙasar (waɗanda ba Isra'ilawa ba ne), 21 wato, waɗanda suka ragu a
ƙasar, waɗanda Isra'ilawa ba su iya hallakawa ba, su ne Solomon ya ɗauka su zama
bayinsa don aikin gandu, kamar yadda yake har wa yau. 22 Amma Solomon bai mai
da Isra'ilawa bayi ba; su ne mayaƙansa, shugabannin gwamnatinsa, dogarawansa,
shugabannin sojojinsa, da shugabanninsa na kekunan yaƙi da mahayan kekunan
yaƙinsa. 23 Su ne kuma manyan shugabanni masu lura da ayyukan Solomon, su ne
shugabanni 550 masu lura da mutanen da suke aiki.

---

[*] **9:13** Kabul ya yi kamar kalmar Ibraniyanci na abu marar amfani. [†] **9:14** Wato, kamar ton 4 da 1/2 ke nan

24 Bayan ʼyar Firʼauna ta haura daga Birnin Dawuda zuwa fadan da Solomon ya
gina mata, sai ya gina madogaran gini.
25 Sau uku a shekara Solomon kan miƙa hadayun ƙonawa da hadayun salama a
kan bagaden da ya gina wa Ubangiji, yana ƙone turare a gaban Ubangiji haɗe da su,
ta haka ya cika abin da ake bukata na haikali.
26 Sarki Solomon ya kuma gina jiragen ruwa a Eziyon Geber, wadda take kusa da
Elot a Edom, a bakin Jan Teku. 27 Hiram kuwa ya aiki mutanensa, masu tuƙan jirgin
ruwa waɗanda suka san teku, don su yi hidima a jerin jiragen ruwa tare da mutanen
Solomon. 28 Suka tafi Ofir suka kuma dawo da talenti 420 na zinariya, wanda suka
ba wa Sarki Solomon.

# 10

*Sarauniyar Sheba ta ziyarci Solomon*
*(2 Tarihi 9.1-12)*

1 Saʼad da sarauniyar Sheba ta ji game da sunan da Solomon ya yi, da kuma
dangantakarsa da Ubangiji, sai ta zo tă gwada shi da tambayoyi masu wuya. 2 Ta
iso Urushalima da tawaga mai yawa, tare da raƙuma masu ɗauke da kayan yaji,
da zinariya masu yawa, da duwatsu masu daraja. Ta zo wurin Solomon ta kuwa yi
magana da shi game da dukan abin da take da shi a ranta. 3 Solomon ya amsa dukan
tambayoyinta, ba abin da ya yi wa sarki wuyan bayyanawa mata. 4 Da sarauniya
Sheba ta ga dukan hikimar Solomon da fadan da ya gina. 5 Da irin abincin da yake
kan teburinsa, da irin zaman fadawansa, da irin rigunan masu hidimarsa, da irin
masu shayarwarsa, da kuma hadayun ƙonawar da yake yi a haikalin Ubangiji, sai ta
yi mamaki ƙwarai.
6 Ta ce wa sarki, “Labarin da na ji a ƙasata game da abin da ka yi da kuma
hikimarka gaskiya ne. 7 Amma ban gaskata waɗannan abubuwa ba sai da na zo
na gani da idanuna. Tabbatacce, ba a ma faɗa mini ko rabi ba. Gama cikin hikima
da arziki, ka wuce labarin da na ji nesa ba kusa ba. 8 Abin farin ciki ne ga mutanenka!
Abin farin ciki ne ga fadawanka, waɗanda suke cin gaba da tsayawa a gabanka suna
kuma jin hikimarka! 9 Yabo ga Ubangiji Allahnka, wanda ya ji daɗinka, ya kuma
sa ka a kujerar sarautar Israʼila. Ubangiji ya naɗa ka sarki saboda madawwamiyar
ƙaunar wa Israʼila, don ka yi shariʼa da adalci.”
10 Ta kuma ba sarki talenti 120 na zinariya, da kayan yaji masu yawa, da kuma
duwatsu masu daraja. Ba a taɓa kawo kayan yaji da yawa haka kamar yadda
sarauniyar Sheba ta ba wa Sarki Solomon ba.
11 (Jiragen ruwan Hiram suka kawo zinariya daga Ofir. Daga can kuma suka kawo
kaya masu yawa na katakon almug, da kuma duwatsu masu daraja. 12 Sarki ya yi
amfani da almug don yă yi kayan ado wa haikalin Ubangiji da kuma don fadan sarki,
don kuma yă yi molaye, da garayu saboda mawaƙa. Ba a taɓa yin jigilar katakon
almug ko a gani irin yawan katakai haka ba har wa yau.)
*(2 Tarihi 9.13-28)*
13 Sarki Solomon ya ba wa sarauniyar Sheba dukan abin da take so, da kuma duk
abin da ta nema, ban da abin da ya ba ta daga yalwar fadan sarki. Saʼan nan ta koma
tare da tawagarta zuwa ƙasarta.

*Daukakar Solomon*

14 Nauyin zinariya da Solomon yake samun kowace shekara, talenti 666 ne. 15 Ban
da haraji daga ʼyan kasuwa, da fatake, da kuma daga dukan sarakunan Arabiya, da
gwamnonin ƙasar.
16 Sarki Solomon ya yi manyan garkuwoyi ɗari biyu na zinariya. An yi kowace
garkuwa da zinariya bekas ɗari shida. 17 Ya kuma yi ƙananan garkuwoyi ɗari uku

na zinariya. An yi kowane garkuwa da zinariya minas uku. Ya sa su a cikin Fadar Kurmin Lebanon.
18 Sa'an nan sarki ya yi kujerar sarauta mai nauyin giram na hauren giwa, aka
kuma dalaye ta da zinariya zalla. 19 Kujera sarautar ta kasance da matakai shida,
kuma bayanta tana da bisa mai kamannin gammo. A kowane gefen kujerar akwai
wurin sa hannu, da kuma zaki tsaye kusa da kowannensu. 20 Zakoki goma sha biyu
suna tsaye a matakai shida, ɗaya a kowane gefen ƙarshen mataki. Babu ƙasar da
an taɓa gina irin wannan kujerar mulki. 21 Dukan kwaf Solomon zinariya ne, kuma
dukan kayayyakin gida a Fadan da ake kira Kurmin Lebanon, zinariya ce zalla. Babu
wani abin da aka yi da azurfa, domin ba a ɗauki azurfa a bakin kome ba a zamanin
Solomon. 22 Sarki yana da jerin jiragen ruwan kasuwanci* a teku, tare da jiragen
ruwan Hiram. Sau ɗaya kowace shekara uku jerin jiragen yakan dawo ɗauke da
zinariya, da azurfa, da hauren giwa, da birai marasa wutsiya, da kuma gogon biri.
23 Sarki Solomon ya yi suna a wadata fiye da dukan sarakunan duniya. 24 Dukan
duniya ta nemi su zo wurin Solomon don su ji hikimar da Allah ya sa a zuciyarsa.
25 Kowace shekara, kowa da ya zo wurinsa yakan kawo kyautai, kayayyakin azurfa
da na zinariya, riguna, makamai, da kayan yaji, dawakai da alfadarai.
26 Solomon ya tara kekunan yaƙi da dawakai; ya kasance da kekunan yaƙi dubu
goma sha huɗu, da dawakai dubu goma sha biyu waɗanda ya ajiye a biranen
kekunan yaƙi, ya kuma ajiye tare da shi a Urushalima. 27 Sarki ya mai da azurfa
barkatai a cikin Urushalima kamar duwatsu, al'ul kuma da yawa kamar itatuwan
fir na jumaiza a gindin tuddai. 28 An yi jigilar dawakan Solomon daga Masar† da
kuma daga Kuye‡, 'yan kasuwan fadan sarki sun sayo su daga Kuye. 29 Suka yi jigilar
kekunan yaƙi daga Masar a bakin shekel ɗari shida na azurfa, doki ɗaya kuma a kan ɗari da hamsin. Sun kuma yi jigilarsu suna sayarwa ga dukan sarakunan Hittiyawa da na Arameyawa.

# 11

*Matan Solomon*

1 Sarki Solomon ya ƙaunaci baƙin mata. Ban da 'yar Fir'auna, ya auri Mowabawa,
Ammonawa, mutanen Edom, Sidoniyawa da Hittiyawa. 2 Sun fito daga al'ummai da
UBANGIJI ya ce wa Isra'ilawa, "Kada ku yi aurayya da su, domin tabbatacce za su
juye zukatanku zuwa ga waɗansu alloli." Duk da haka Solomon ya manne musu, ya
nace, yana ƙaunarsu. 3 Ya auri mata ɗari bakwai, haifaffun gidan sarauta, da kuma
ƙwarƙwarai ɗari uku. Matan nan nasa suka karkatar da shi. 4 Yayinda Solomon yake
tsufa, matansa suka juye zuciyarsa ga bin waɗansu alloli, zuciyarsa kuwa ba tă bi
UBANGIJI Allahnsa ɗungum kamar yadda zuciyar Dawuda mahaifinsa ta kasance ba.
5 Ya bi Ashtarot, alliyar Sidoniyawa, da Molek*, allahn da aka hana na Ammonawa.
6 Saboda haka Solomon ya yi abin da yake mugu a gaban UBANGIJI. Bai bi UBANGIJI
gaba ɗaya kamar yadda Dawuda mahaifinsa ya yi ba.
7 A kan tudu, gabas da Urushalima, Solomon ya gina masujada a can domin Kemosh,
allahn da aka hana na Mowab, da Molek, allahn da aka hana na Ammonawa. 8 Ya
yi haka domin dukan baƙin matansa, waɗanda suka ƙone turare suka kuma miƙa hadayu ga allolinsu.
9 UBANGIJI ya yi fushi da Solomon domin zuciyarsa ya juye daga UBANGIJI, Allah
na Isra'ila, wanda ya bayyana masa sau biyu. 10 Ko da yake ya hana Solomon bin
waɗansu alloli, Solomon bai kiyaye umarnin UBANGIJI ba. 11 Saboda haka UBANGIJI

* **10:22** Da Ibraniyanci na jiragen Tarshish † **10:28** Mai yiwuwa Muzur, wani yanki a Silisiya; haka ma a aya 29. ‡ **10:28** Mai yiwuwa Silisiya * **11:5** Da Ibraniyanci Milkom; haka ma a aya 33.

ya ce wa Solomon, “Da yake halinka ke nan, ba ka kuma kiyaye alkawarina, da
ƙaʼidodina da na umarce ka ba, tabbatacce zan yage masarautar daga gare ka, in ba
da ita ga ɗaya daga cikin bayinka. 12 Amma saboda Dawuda mahaifinka, ba zan yi
haka a zamaninka ba. Zan yage ta daga hannun ɗanka. 13 Amma ba zan yage dukan
masarautar daga gare shi ba, zan ba shi kabila ɗaya saboda Dawuda bawana, da
kuma saboda Urushalima, wadda na zaɓa.”

### *Abokan gāban Solomon*

14 Sai UBANGIJI ya tayar wa Solomon wani abokin gāba, mai suna Hadad, mutumin
Edom daga gidan sarautar Edom. 15 A shekarun baya Dawuda ya ci Edom da yaƙi.
Yowab, shugaban sojojinsa ya tafi can domin yǎ binne Israʼilawa waɗanda suka mutu
a yaƙi. Saʼad da suke a can, sojojin Israʼila suka kashe kowane ɗa namiji a Edom.
16 Yowab da dukan Israʼilawa suka zauna a can, wata shida, sai da suka hallaka dukan
mutane a Edom. 17 Amma Hadad yana ɗan yaro a lokaci, wanda ya gudu zuwa Masar
tare da shugabannin mutanen Edom waɗanda suka yi wa mahaifinsa hidima. 18 Suka
taso daga Midiyan suka tafi Faran. Saʼan nan suka ɗauki mutane daga Faran suka tafi
Masar, zuwa wurin Firʼauna wanda ya ba wa Hadad gida da ƙasa, ya kuma tanada
masa da abinci.
19 Firʼauna ya ji daɗin Hadad har ya ba shi ʼyarʼuwar matarsa, Sarauniya Tafenes,
aure. 20 ʼYarʼuwar Tafenes ta haifi masa ɗa wanda ya kira Genubat, wanda Tafenes
ta yi renonsa a fadan sarki. A can, Genubat ya yi zama da ʼyaʼyan Firʼauna.
21 Yayinda yake a Masar, Hadad ya ji Dawuda ya huta tare da kakanninsa, ya kuma
ji cewa Yowab shugaban mayaƙa ya mutu. Sai Hadad ya ce wa Firʼauna, “Bari in tafi,
don in koma ƙasata.”
22 Firʼauna ya tambaye shi, ya ce, “Me ka rasa a nan da kake so ka koma garinka?”
Ya ce, “Ba kome, amma ka dai bar ni in tafi!”
23 Allah kuwa ya tayar wa Solomon wani abokin gāba, mai suna Rezon, ɗan Eliyada,
wanda ya gudu daga maigidansa, Hadadezer sarkin Zoba. 24 Rezon ya tattara mutane
kewaye da shi, ya zama kuma shugaban ʼyan tawaye saʼad da Dawuda ya hallaka
mayaƙan Zoba; ʼyan tawayen suka tafi Damaskus, inda suka zauna, suka kuma yi
mulki. 25 Rezon ya zama babban abokin gāban Israʼila cikin dukan kwanakin mulkin
Solomon. Ya ƙara rikici a kan rikicin Hadad. Rezon ya ƙi mulkin Israʼila da dukan
ransa. Saboda haka Rezon ya yi mulki a Aram ya kuma ƙi jinin Israʼila.

### *Yerobowam ya yi wa Solomon tawaye*

26 Haka ma Yerobowam, ɗan Nebat, shi ma ya yi wa sarki tawaye. Shi ɗaya ne
daga shugabannin Solomon, shi mutumin Efraim ne daga Zereda, mahaifiyarsa kuwa
gwauruwa ce, mai suna Zeruwa.
27 Ga yadda ya tayar wa sarki Solomon. Sarki Solomon ya gina madogaran gini†,
ya ciccika wurare a katangar birnin Dawuda mahaifinsa da ƙasa. 28 To, Yerobowam
mutum ne mai fasaha. Saʼad da Solomon ya ga yadda matashin yake aiki da himma,
sai ya sa shi yǎ lura da dukan aikin gandu na gidan Yusuf.
29 Da Yerobowam ya fita Urushalima, sai annabi Ahiya, mutumin Shilo ya tarar da
shi a hanya. Lokacin kuwa Ahiya yana saye da sabuwar riga, ba kowa a filin sai
su biyu kaɗai. 30 Sai Ahiya ya kama sabuwar rigar da yake saye da ita ya yage ta
gida goma sha biyu. 31 Saʼan nan ya ce wa Yerobowam, “Dauki gida goma wa kanka,
gama abin da UBANGIJI, Allah na Israʼila ya ce ke nan, ʻDuba, zan yage masarauta daga
hannun Solomon in ba ka kabilu goma. 32 Amma saboda bawana Dawuda da kuma
birnin Urushalima, wadda na zaɓa daga dukan kabilan Israʼila, zai sami kabila guda.
33 Zan yi wannan domin sun yashe ni, suka kuma yi wa Ashtarot, alliyar Sidoniyawa,

† **11:27** Ko kuwa Millo

da Kemosh, allahn Mowabawa, da kuma Molek, allahn Ammonawa sujada, ba su yi
tafiya a hanyoyina ba, ba su kuwa yi abin da yake daidai a idanuna ba, ba su kiyaye
farillaina da dokokina kamar yadda Dawuda, mahaifin Solomon ya yi ba.
34 “ ‘Amma ba zan ɗauki dukan masarautar daga hannun Solomon ba; na naɗa shi
sarki, dukan kwanaki ransa saboda Dawuda bawana, wanda na zaɓa, wanda kuma
ya kiyaye umarnai da farillaina. 35 Zan ɗauke masarautar daga hannuwan ɗansa ne,
in ba ka kabilu goma. 36 Zan ba da ɗaya ga ɗansa don kullum Dawuda bawana yă
kasance da fitila a gabana a Urushalima, birnin da na zaɓa in sa Sunana. 37 Amma fa,
ga kai, zan ɗauke ka, za ka kuwa yi mulki bisa dukan abin da zuciyarka take so; za
ka zama sarki a bisa Isra’ila. 38 In ka aikata dukan abin da na umarce ka, ka yi tafiya
a hanyoyina, ka kuma yi abin da yake daidai a idanuna ta wurin kiyaye farillaina da
umarnaina, kamar yadda Dawuda bawana ya yi, zan kasance tare da kai. Zan gina
maka masarauta mai dawwama kamar wadda na gina wa Dawuda, zan kuma ba da
Isra’ila gare ka. 39 Zan ƙasƙantar da zuriyar Dawuda saboda wannan, amma ba har
abada ba.’ ”
40 Solomon ya yi ƙoƙari yă kashe Yerobowam, amma Yerobowam ya tsere zuwa
Masar, zuwa wurin sarki Shishak, ya zauna a can sai bayan mutuwar Solomon.

### *Mutuwar Solomon*
### *(2 Tarihi 9.29-31)*

41 Game da sauran ayyukan mulkin Solomon, da dukan abubuwan da ya yi, da
hikimar da ya nuna, an rubuta su a littafin tarihin Solomon. 42 Solomon ya yi mulki
a Urushalima, a bisa dukan Isra’ila, shekaru arba’in. 43 Sa’an nan ya huta tare da
kakanninsa, aka kuma binne shi a birnin Dawuda mahaifinsa. Sai Rehobowam ɗansa
ya gāje shi a matsayin sarki.

# 12

### *Isra’ilawa sun yi wa Rehobowam tawaye*
### *(2 Tarihi 10.1-19)*

1 Rehobowam ya tafi Shekem, gama dukan Isra’ila sun je can don su naɗa shi sarki.
2 Sa’ad da Yerobowam ɗan Nebat ya ji labari (gama har yanzu yana a Masar, inda ya
gudu daga Sarki Solomon), sai ya dawo daga Masar. 3 Saboda haka mutane suka aika
Yerobowam yă zo, sai shi da dukan taron Isra’ila suka tafi wurin Rehobowam, suka
ce masa, 4 “Mahaifinka ya sa mana kaya mai nauyin gaske, amma yanzu ka sassauta
wannan aiki mai zafi, da kuma kaya masu nauyin da ya sa a kanmu, mu kuwa za
mu bauta maka.”
5 Rehobowam ya amsa, “Ku tafi, bayan kwana uku, ku dawo.” Sai mutane suka
watse.
6 Sai Sarki Rehobowam ya nemi shawarar dattawa waɗanda suka yi wa mahaifinsa
Solomon, hidima a kwanakinsa. Ya ce, “Wace shawara ce za ku ba ni don in amsa
wa waɗannan mutane?”
7 Suka amsa, “In a yau za ka zama bawan waɗannan mutane, ka kuma yi musu
hidima, ka ba su amsa mai kyau, kullum za su kasance bayinka.”
8 Amma Rehobowam ya ƙi shawarar da dattawan suka ba shi, sai ya nemi shawarar
matasa waɗanda suka yi girma tare, waɗanda kuma suke masa hidima. 9 Ya tambaye
su, “Mece ce shawararku? Yaya za mu amsa wa waɗannan mutane masu cewa, ‘Ka
sassauta nauyin da mahaifinka ya sa a kanmu’?”
10 Matasan, waɗanda suka yi girma tare da shi, suka amsa, “Faɗa wa waɗannan
mutanen da suka ce maka, ‘Mahaifinka ya sa kaya masu nauyi a kanmu, amma
ka sassauta kayanka.’ Ka ce musu, ‘Karamin yatsana ya fi ƙugun tsohona kauri.
11 Mahaifina ya sa muku kaya masu nauyi; ni zan ma sa su fi haka nauyi. Mahaifina
ya hore ku da bulala; ni kuwa zan hore ku da kunamai.’ ”

12 Bayan kwana uku, Yerobowam da dukan mutane suka dawo wurin Rehobowam
yadda sarki ya faɗa, “Ku dawo gare ni cikin kwana uku.” 13 Sai Sarki ya amsa wa
mutane da zafi. Yana ƙin shawarar da dattawa suka ba shi. 14 Ya bi shawarar matasa,
ya ce, “Mahaifina ya sa muku kaya masu nauyi; ni zan ma sa su fi haka nauyi.
Mahaifina ya hore ku da bulala; ni kuwa zan hore ku da kunamai.” 15 Saboda haka
sarki bai saurare mutane ba, gama wannan abin da ya faru daga wurin UBANGIJI ne,
don a cika maganar UBANGIJI da ya yi wa Yerobowam ɗan Nebat ta wurin Ahiya,
mutumin Shilo.
16 Da dukan Isra'ila suka ga sarki ya ƙi yǎ saurare su, sai suka amsa wa sarki,
“Ina ruwanmu da Dawuda!
Ai! Ba mu da gādo wurin ɗan Yesse.
Ya Isra'ila, kowa yǎ koma tentinsa!
Dawuda, sai ka lura da gidanka!”
Saboda haka Isra'ilawa suka watse zuwa gida. 17 Amma ga Isra'ilawan da suke zama
a garuruwan Yahuda kuwa, Rehobowam ya ci gaba da mulki a kansu.
18 Sarki Rehobowam ya aiki Adoniram wanda yake shugaban aikin gandu, amma
Isra'ila suka jajjefe shi da dutse har ya mutu. Sarki Rehobowam, ya sullale ya hau
keken yaƙinsa ya tsere zuwa Urushalima. 19 Tun daga wannan ranar ne mutanen
Isra'ila suka shiga gāba da gidan Dawuda har wa yau.
20 Sa'ad da dukan Isra'ilawa suka ji Yerobowam ya dawo, sai suka aika, suka kira
shi zuwa taro, suka kuma naɗa shi sarki bisa dukan Isra'ila. Kabila Yahuda kaɗai ta
kasance mai biyayya ga gidan Dawuda.

*(2 Tarihi 11.1-4)*

21 Da Rehobowam ya isa Urushalima, ya tattara dukan gidan Yahuda da kabilar
Benyamin, ya sami sun kai mayaƙa dubu da tamanin. Sai aka shirya don su yaƙi
gidan Isra'ila, su kuma mayar da masarautar wa Rehobowam ɗan Solomon.
22 Amma waɗannan kalmomin Allah suka zo wa Shemahiya, mutumin Allah, cewa,
23 “Faɗa wa Rehobowam ɗan Solomon, sarkin Yahuda, ka faɗa wa dukan gidan
Yahuda da Benyamin, da kuma dukan sauran mutane, 24 ‘Ga abin da UBANGIJI ya
ce, “Kada ku haura don ku yi yaƙi da 'yan'uwanku, Isra'ilawa. Ku koma gida,
kowannenku, gama wannan aikina ne.” ’ ” Saboda haka suka yi biyayya da maganar
UBANGIJI, suka sāke watse zuwa gida, yadda UBANGIJI ya umarta.

### *'Yan maruƙan zinariya a Betel da Dan*

25 Sai Yerobowam ya ƙara gina Shekem a ƙasar tudu ta Efraim, ya zauna a can.
Daga can ya tafi ya gina Fenuwel.
26 Yerobowam ya yi tunani a ransa ya ce, “Mai yiwuwa mulkin yǎ koma gidan
Dawuda. 27 In waɗannan mutane sun riƙa haurawa don su miƙa hadayu a haikalin
UBANGIJI a Urushalima. Za su sāke nuna biyayya ga mai girma, Rehobowam, sarkin
Yahuda. Za su kashe ni su kuma koma ga Sarki Rehobowam.”
28 Bayan ya nemi shawara, sai sarki ya yi siffofin 'yan maruƙa biyu na zinariya.
Ya ce wa mutane, “Kun daɗe kuna haurawa zuwa can Urushalima. Ga allolinku, ya
Isra'ila, waɗanda suka fitar da ku daga ƙasar Masar.” 29 Sai ya kafa ɗaya a Betel,
ɗaya kuma a Dan. 30 Wannan ya zama zunubi, gama mutane suna tafiya yin wa
wannan da yake a Betel sujada, su kuma je har Dan don su yi wa ɗayan sujada.
31 Yerobowam ya gina masujadai da suke kan tuddai, ya kuma naɗa firistoci
barkatai daga cikin mutanen da ba na zuriyar Lawi ba. 32 Ya kafa biki a rana ta
goma sha biyar ta watan takwas, kamar bikin da ake yi a Yahuda, ya kuma miƙa
hadayu a bisa bagade. Ya yi haka a Betel, yana miƙa wa siffofin maruƙan da ya yi
hadayu. A Betel kuma ya naɗa firistoci a wuraren tudun da ya yi. 33 A rana ta goma
sha biyar ta watan takwas, watan da ya zaɓa, ya miƙa hadayu a bisa bagaden da ya

gina a Betel. Saboda haka ya kafa biki don Isra'ilawa, ya kuma haura zuwa bagade
don yă miƙa hadayu.

# 13

*Mutumin Allah daga Yahuda*

1 Bisa ga umarnin Ubangiji, sai wani mutumin Allah ya zo daga Yahuda zuwa Betel,
yayinda Yerobowam yake tsaye kusa da bagade don yă miƙa hadaya. 2 Sai mutumin
Allah ya tā da murya a kan bagade bisa ga umarnin Ubangiji ya ce, "Ya bagade,
bagade! Ubangiji ya ce, 'Za a haifi ɗa mai suna Yosiya wa gidan Dawuda. A kanka
zai miƙa firistoci na masujadai kan tuddai masu miƙa hadayu a nan, za a kuma ƙone
ƙasusuwan mutane a kanka.' " 3 A wannan rana mutumin Allah ya ba da alama, "Ga
alamar da Ubangiji ya furta. Wannan bagade zai tsage yă rabu kashi biyu, tokar da
yake a kansa za tă zuba a ƙasa."

4 Sa'ad da Yerobowam ya ji abin da mutumin Allah ya tā da murya ya faɗa game
da bagaden Betel, sai ya miƙa hannunsa daga bagaden ya ce, "Ku kama shi!" Amma
sai hannun da ya miƙa ya yanƙwane, har bai iya janye shi ba. 5 Haka ma, bagaden
ya rabu, tokarsa kuma ya zuba, bisa ga alamar da mutumin Allah ya bayar, ta wurin
kalmar Ubangiji.

6 Sai sarki ya ce wa mutumin Allah, "Ka roƙi Ubangiji Allahnka, ka kuma yi addu'a
domina don hannuna ya warke." Saboda haka mutumin Allah ya yi roƙo ga Ubangiji,
hannun sarki kuwa ya warke, ya kuma zama kamar yadda yake a dā.

7 Sai sarki ya ce wa mutumin Allah, "Zo gida tare da ni, ka sami wani abu ka ci,
zan kuwa yi maka kyauta."

8 Amma mutumin Allah ya amsa wa sarki, "Ko da za ka ba rabin mallakarka, ba
zan tafi tare da kai ba, ba kuwa zan ci abinci, ko in sha ruwa a can ba. 9 Gama an
umarce ni ta wurin kalmar Ubangiji, aka ce, 'Kada ka ci abinci, ko ka sha ruwa, ko
ka koma ta hanyar da ka zo.' " 10 Saboda haka ya ɗauki wata hanya, bai kuwa koma
ta hanyar da ya zo Betel ba.

11 To, fa, akwai wani tsohon annabi yana zama a Betel, wanda 'ya'yansa suka zo
suka faɗa masa dukan abin da mutumin Allah ya yi a can, a ranar. Suka kuma
faɗa wa mahaifinsu abin da ya faɗa wa sarki. 12 Mahaifinsu ya tambaye su ya ce,
"Wace hanya ce ya bi?" Sai 'ya'yansa suka nuna masa hanyar da mutumin Allah
daga Yahuda ya bi. 13 Sai ya ce wa 'ya'yansa, "Ku yi wa jakina shimfiɗa." Da suka yi
wa jakin shimfiɗa, sai ya hau. 14 Ya bi bayan mutumin Allah. Ya same shi yana zama
a ƙarƙashin itace oak, sai ya tambaye shi ya ce, "Kai ne mutumin Allah wanda ya zo
daga Yahuda?"

Ya amsa, "Ni ne."

15 Saboda haka annabin ya ce masa, "Zo gida tare da ni ka ci abinci."

16 Mutumin Allah ya ce, "Ba zan koma tare da kai ba, ko in ci abinci, ko in sha ruwa
tare da kai a can ba. 17 An faɗa mini ta wurin maganar Ubangiji, 'Kada ka ci abinci,
ko ka sha ruwa a can, ko ka koma ta hanyar da ka zo.' "

18 Sai annabin ya amsa, "Ni ma annabi ne, kamar ka. Kuma mala'ika ya ce mini
ta wurin kalmar Ubangiji, 'Dawo da shi zuwa gidanka saboda yă ci abinci, yă kuma
sha ruwa.' " (Amma yana masa ƙarya ne.) 19 Sai mutumin Allah ya koma tare da shi
ya kuma ci ya sha a gidansa.

20 Yayinda suke zaune a teburi, sai maganar Ubangiji ta zo wa tsohon annabin da
ya dawo da mutumin Allah. 21 Sai tsohon annabin ya tā da murya wa mutumin Allah
wanda ya zo daga Yahuda, "Ga abin da Ubangiji ya ce, 'Ka ƙazantar da maganar
Ubangiji, ba ka kuma kiyaye umarnin Ubangiji Allahnka ba. 22 Ka dawo ka ci abinci,

ka kuma sha ruwa a wurin da na faɗa maka kada ka ci, ko ka sha. Saboda haka ba
za a binne jikinka a kabarin kakanninka ba.' "

23 Sa'ad da mutumin Allah ya gama ci da sha, sai annabin da ya dawo da shi ya yi
wa jakin mutumin Allah shimfiɗa. 24 Yayinda yake kan hanyarsa, sai wani zaki ya
sadu da shi ya kashe shi, aka kuma jefar da jikinsa a kan hanya, jakin da zakin suka
tsaya kusa da gawar. 25 Waɗansu mutane masu wucewa suka ga an yar da gawar
a can, zaki yana tsaye kusa da gawar, sai suka tafi suka ba da labarin a birni inda
tsohon annabin nan yake zama.

26 Sa'ad da annabin da ya dawo da mutumin Allah ya ji, sai ya ce, "Mutumin Allah
ne, wanda ya ƙazantar da maganar UBANGIJI. UBANGIJI ya bashe shi ga zaki, wanda
ya yayyage shi ya kuma kashe shi, kamar yadda maganar UBANGIJI ta gargaɗe shi."

27 Sai annabin ya ce wa 'ya'yansa, "Ku yi wa jakina shimfiɗa." Sai suka yi. 28 Sai
ya fita ya sami an jefar da gawar a hanya, jakin da zakin suna tsaye kusa da shi.
Zakin bai ci gawar ko yă yayyage jakin ba. 29 Saboda haka annabin ya ɗauki gawar
mutumin Allah, ya shimfiɗa shi a kan jaki, ya koma da shi cikin birninsa don yă
yi makokinsa yă kuma binne shi. 30 Sai ya kwantar da gawar a kabarinsa, suka yi
makoki a kansa, ya kuma ce, "Ayya, abokina!"

31 Bayan an binne shi, sai ya ce wa 'ya'yansa, "Sa'ad da na mutu, ku binne
ni a kabarin da aka binne mutumin Allah; ku kwantar da ƙasusuwana kusa da
ƙasusuwansa. 32 Gama annabcin da ya yi ta maganar UBANGIJI gāba da bagaden
da yake cikin Betel da kuma wuraren sujada a tuddan da suke a biranen Samariya,
ba shakka zai cika."

33 Har ma bayan wannan, Yerobowam bai canja daga mugayen hanyoyinsa ba,
amma ya ƙara naɗa firistoci domin masujadai da suke kan tuddai daga kowane irin
mutane. Duk wanda ya so yă zama firist sai yă naɗa shi don aiki a masujadai da
suke kan tuddai. 34 Wannan ne zunubin gidan Yerobowam da ya kai ga fāɗuwarsa
da kuma hallakarsa daga fuskar duniya.

# 14

*Annabcin Ahiya a kan Yerobowam*

1 A lokacin Abiya, ɗan Yerobowam ya kamu da ciwo, 2 sai Yerobowam ya ce wa
matarsa, "Ki tafi, ki ɓad da kama, don kada a gane ke a matsayin matar Yerobowam.
Ki je Shilo. Annabi Ahiya yana a can, wannan wanda ya ce mini zan zama sarki a
bisa wannan mutane. 3 Ki ɗauki dunƙulen burodi goma tare da ke, da waina, da
tulun zuma, ki tafi wurinsa. Zai faɗa miki abin da zai faru da yaron." 4 Saboda haka
matar Yerobowam ta yi abin da ya faɗa, ta kuma tafi gidan Ahiya a Shilo.

Yanzu dai Ahiya ba ya gani; idanunsa sun tafi saboda tsufa. 5 Amma UBANGIJI ya ce
wa Ahiya, "Matar Yerobowam tana zuwa tă tambaye ka game da ɗanta, gama yana
ciwo, za ka kuwa ba ta amsa kaza da kaza. Sa'ad da ta iso za tă yi kamar wata ce
dabam."

6 Saboda haka sa'ad da Ahiya ya ji motsin sawunta a ƙofa, sai ya ce, "Ki shigo, matar
Yerobowam. Me ya sa kike yi kamar wata ce dabam? An aiko ni wurinki da labari
marar daɗi. 7 Je ki faɗa wa Yerobowam cewa ga abin da UBANGIJI, Allah na Isra'ila ya
ce, 'Na tā da kai daga cikin mutane, na mai da kai shugaba a bisa mutanena Isra'ila.
8 Na yage mulki daga gidan Dawuda na ba da shi gare ka, amma ba ka zama kamar
bawana Dawuda wanda ya kiyaye umarnaina ya kuma bi ni da dukan zuciyarsa,
yana yin abin da yake daidai kaɗai a idanuna ba. 9 Ka aikata mugunta fiye da dukan
waɗanda suka rayu kafin kai. Ka yi wa kanka waɗansu alloli, gumakan da aka yi da
ƙarfe; ka tsokane ni na yi fushi, ka kuma juye mini baya.

10 “ ‘Saboda wannan, zan kawo masifa a gidan Yerobowam. Zan yanke kowane ɗa
na ƙarshe a Isra'ila, bawa ko 'yantacce. Zan ƙone gidan Yerobowam kamar yadda
mutum yakan ƙone juji, sai duk ya ƙone ƙurmus. 11 Karnuka za su ci waɗanda
suka mutu na Yerobowam a cikin birni, kuma tsuntsayen sararin sama za su cinye
waɗanda suka mutu a jeji. Ni Ubangiji na faɗa!’
12 “Ke kuma, ki koma gida. Sa'ad da kika taka ƙafa a birninki, yaron zai mutu.
13 Dukan Isra'ila kuwa za su yi makoki dominsa. Shi ne kaɗai na Yerobowam wanda
za a binne, domin shi ne kaɗai a gidan Yerobowam wanda Ubangiji, Allah na Isra'ila
ya sami wani ɗan abu mai kyau a kansa.
14 “Ubangiji zai tā da wani sarki wa kansa a bisa Isra'ila wanda zai hallaka iyalin
Yerobowam. Ko yanzu ma, wannan zai fara faruwa. 15 Ubangiji kuma zai bugi
Isra'ila, har tă zama kamar kyauro mai girgiza a bakin rafi. Zai tumɓuke Isra'ila
daga wannan ƙasa mai kyau da ya ba wa kakanninsu, yă watsar da su gaba da Kogin
Yuferites domin sun tsokane Ubangiji har ya yi fushi, ta wurin yin ginshiƙan Ashera.
16 Zai kuma ba da Isra'ila saboda zunuban da Yerobowam ya yi, da ya kuma sa Isra'ila
suka yi.”
17 Sai matar Yerobowam ta tashi ta tafi, ta kuwa tafi Tirza. Nan da nan da ta taka
madogarar ƙofar gidan, sai yaron ya mutu. 18 Suka binne shi, dukan Isra'ila kuwa
suka yi makoki dominsa, yadda Ubangiji ya faɗa ta wurin bawansa annabi Ahiya.
19 Sauran ayyukan sarautar Yerobowam, da yaƙe-yaƙensa, da yadda ya yi mulki, ba
a rubuce suke a littafin tarihi na sarakunan Isra'ila ba? 20 Ya yi mulki shekaru ashirin
da biyu, sai ya huta tare da kakanninsa. Sai Nadab ɗansa ya gāje shi a matsayin sarki.

### *Rehobowam sarkin Yahuda*
### *(2 Tarihi 11.5–12.16)*

21 Rehobowam ɗan Solomon ya zama sarki a Yahuda. Yana da shekara arba'in
da ɗaya sa'ad da ya zama sarki, ya kuma yi mulki shekaru goma sha bakwai a
Urushalima, birnin da Ubangiji ya zaɓa daga cikin dukan kabilan Isra'ila don yă
sa Sunansa. Sunan mahaifiyarsa Na'ama, ita mutuniyar Ammon ce.
22 Yahuda ya aikata mugunta a gaban Ubangiji. Ta wurin zunuban da suka yi,
sun tā da fushin kishinsa fiye da yadda kakanninsu suka yi. 23 Sun kuma kafa wa
kansu masujadai da suke kan tuddai, da a kan keɓaɓɓun duwatsu, suka kuma gina
ginshiƙan Ashera a kowane tudu, da kuma a ƙarƙashin kowane duhuwar itace. 24 Har
ma akwai maza karuwai na masujada. Mutane suka sa kansu ga yin kowane abin
ƙyama na al'umman da Ubangiji ya kora kafin Isra'ilawa.
25 A shekara ta biyar ta Sarki Rehobowam, Shishak sarkin Masar ya kai wa
Urushalima yaƙi. 26 Ya kwashe dukiyar haikalin Ubangiji da kuma dukiyar fadan
sarki. Ya ɗauki kome, har da dukan garkuwoyi na zinariya da Solomon ya yi.
27 Saboda haka sarki Rehobowam ya yi garkuwoyin tagulla ya mayar da su. Ya kuma
naɗa waɗannan shugabannin matsara ya sa su aiki a ƙofar zuwa fadan sarki. 28 Duk
sa'ad da sarki ya tafi wurin haikalin Ubangiji, matsara sukan riƙe garkuwoyinsu,
daga baya kuma sai su mai da su ɗakin tsaro.
29 Game da sauran ayyukan mulkin Rehobowam kuwa, da kuma dukan abin da
ya yi, duk a rubuce suke a cikin littafin tarihin sarakunan Yahuda. 30 Aka ci gaba
da yaƙe-yaƙe tsakanin Rehobowam da Yerobowam. 31 Sai Rehobowam ya huta da
kakanninsa, aka kuma binne shi tare da su a Birnin Dawuda. Sunan mahaifiyarsa
Na'ama, ita kuwa mutuniyar Ammon ce. Sai Abiyam[*] ɗansa ya gāje shi a matsayin
sarki.

---

[*] **14:31** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na Ibraniyanci da Seftuwajin (duba kuma 2Tar 12.16); yawancin rubuce-rubucen hannu na Ibraniyanci suna da Abiya

# 15

*Abiya sarkin Yahuda*
*(2 Tarihi 13.1-22)*

1 A shekara ta goma sha takwas ta mulkin Yerobowam ɗan Nebat, Abiyam ya zama
sarkin Yahuda, 2 ya kuma yi mulki a Urushalima shekara uku. Sunan mahaifiyarsa
Ma'aka ne, 'yar Abisalom.

3 Shi ma ya aikata dukan irin zunubai da tsohonsa ya yi. Zuciyarsa ba tă bi Ubangiji
Allahnsa, kamar yadda zuciyar Dawuda kakansa ta yi ba. 4 Duk da haka, saboda
Dawuda Ubangiji Allahnsa ya ba shi fitila a Urushalima ta wurin ta da wani da ya
gāje shi, ta wurinsa kuma Urushalima ta yi ƙarfi. 5 Gama Dawuda ya yi abin da
yake daidai a gaban Ubangiji, bai kuma fasa kiyaye wani daga umarnan Ubangiji ba
dukan kwanakinsa, sai dai a batun Uriya mutumin Hitti.

6 Aka yi yaƙi tsakanin Rehobowam da Yerobowam a duk kwanakin Abiya. 7 Game
da sauran ayyukan mulkin Abiyam kuwa, duk a rubuce suke a cikin littafin tarihin
sarakunan Yahuda. Aka yi yaƙi tsakanin Abiyam da Yerobowam. 8 Sai Abiyam ya
huta tare da kakanninsa, aka kuma binne shi a Birnin Dawuda. Asa kuwa ya gāje
shi a matsayin sarki.

*Asa sarkin Yahuda*
*(2 Tarihi 15.16–16.6,11-13)*

9 A shekara ta ashirin ta Yerobowam sarkin Isra'ila, Asa ya zama sarkin Yahuda,
10 ya yi mulki a Urushalima shekara arba'in da ɗaya. Sunan mahaifiya mahaifiyarsa,
Ma'aka ne 'yar Abisalom.

11 Asa ya yi abin da yake daidai a gaban Ubangiji, kamar yadda kakansa Dawuda
ya yi. 12 Ya kori dukan maza karuwai na masujadai daga ƙasar, ya kuma yi waje da
dukan gumakan da mahaifinsa ya yi. 13 Ya tuɓe mahaifiya mahaifiyarsa Ma'aka daga
matsayinta na mahaifiyar sarauniya, gama ta gina ƙazantaccen ginshiƙin Ashera.
Asa ya yanke ginshiƙin, ya kuma ƙone shi a Kwarin Kidron. 14 Ko da yake bai
cire masujadai da suke kan tuddai ba, zuciyar Asa ta kasance da aminci ɗungum
ga Ubangiji dukan kwanakinsa. 15 Ya kawo azurfa da zinariya da kayayyakin da shi
da mahaifinsa suka keɓe a haikalin Ubangiji.

16 Aka yi yaƙi tsakanin Asa da Ba'asha sarkin Isra'ila dukan kwanakin mulkinsu.
17 Ba'asha sarkin Isra'ila ya haura, ya yi yaƙi da Yahuda, ya kuma gina Rama don yă
hana wani daga fita ko shiga yankin Asa, sarkin Yahuda.

18 Sai Asa ya ɗauki dukan azurfa da kuma zinariyar da suka rage a ma'ajin haikalin
Ubangiji da kuma nasa fadan, ya ba da su ga wani shugabansa, ya kuma aika da su
zuwa ga Ben-Hadad ɗan Tabrimmon, ɗan Heziyon, sarkin Aram, wanda yake mulki
a Damaskus. 19 Ya ce, "Bari yarjejjeniya ta kasance tsakanina da kai, kamar yadda ta
kasance tsakanin mahaifina da mahaifinka. Duba, ina aika maka kyautai na azurfa
da na zinariya. Yanzu fa sai ka janye yarjejjeniyarka da Ba'asha sarkin Isra'ila, don
yă janye daga gare ni."

20 Ben-Hadad ya yarda da maganar Sarki Asa, ya kuma aika shugabannin sojojin
mayaƙansa ya yi yaƙi da garuruwan Isra'ila. Ya kame Iyon, Dan, Abel-Bet-Ma'aka
da dukan Kinneret, haɗe da Naftali. 21 Da Ba'asha ya ji haka, sai ya daina ginin
Rama, ya janye zuwa Tirza. 22 Sai Sarki Asa ya ba da umarni ga dukan Yahuda, kuma
babu wanda aka ware, kowa yă taimaka a kwashe duwatsu da katakan da Ba'asha
yake amfani da su daga Rama. Da duwatsu da katakan ne Sarki Asa ya gina Geba a
Benyamin da kuma Mizfa.

23 Game da sauran ayyukan mulkin Asa, dukan nasarorinsa, dukan abin da ya yi,
da kuma biranen da ya gina, duk a rubuce suke a cikin littafin tarihin sarakunan

Yahuda. A tsufansa, sai ƙafafunsa suka kamu da cuta. 24 Sai Asa ya huta tare da
kakanninsa, aka kuma binne shi tare da su a birnin kakansa Dawuda. Sai Yehoshafat
ɗansa ya gāje shi a matsayin sarki.

### *Nadab sarkin Isra'ila*

25 Nadab ɗan Yerobowam ya zama sarkin Isra'ila a shekara ta biyu ta Asa sarkin
Yahuda, ya kuma yi mulki a bisa Isra'ila shekara biyu. 26 Ya yi mugunta a gaban
UBANGIJI, yana tafiya a hanyoyin mahaifinsa da kuma cikin zunubinsa, wanda ya sa
Isra'ila suka yi.
27 Ba'asha ɗan Ahiya na gidan Issakar ya yi maƙarƙashiya gāba da shi, ya buge shi
a Gibbeton, a wani garin Filistiyawa, yayinda Nadab da dukan Isra'ila suke wa garin
kwanto. 28 Ba'asha ya kashe Nadab a shekara ta uku ta Asa sarkin Yahuda, ya kuma
gāje shi a matsayin sarki.
29 Nan da nan da ya fara mulki, sai ya kashe dukan iyalin Yerobowam. Bai bar wa
Yerobowam wani da rai ba, amma ya hallaka su duka, bisa ga maganar UBANGIJI da
ya ba wa bawansa Ahiya, mutumin Shilo. 30 Wannan abu ya faru saboda zunuban da
Yerobowam ya yi, ya kuma sa Isra'ila ya yi, kuma saboda ya tsokane UBANGIJI, Allah
na Isra'ila, ya yi fushi.
31 Game da sauran ayyukan mulkin Nadab da kuma dukan abin da ya yi, duk a
rubuce suke a cikin littafin tarihin sarakunan Isra'ila. 32 Aka yi yaƙi tsakanin Asa da
Ba'asha sarkin Isra'ila dukan kwanakin mulkinsu.

### *Ba'asha sarkin Isra'ila*

33 A shekara ta uku ta Asa sarkin Yahuda, Ba'asha ɗan Ahiya ya zama sarkin dukan
Isra'ila a Tirza, ya kuma yi sarauta shekara ashirin da huɗu. 34 Ya aikata mugunta a
gaban UBANGIJI, yana tafiya a hanyoyin Yerobowam da kuma cikin zunubinsa, wanda
ya sa Isra'ila suka yi.

## 16

1 Sai maganar UBANGIJI ta zo wa Yehu ɗan Hanani game da Ba'asha, 2 "Na ɗaga ka
daga ƙura na mai da kai shugaban mutanena Isra'ila, amma ka yi tafiya a hanyoyin
Yerobowam, ka kuma sa mutanena Isra'ila suka yi zunubi, ka tsokane ni na yi fushi
ta wurin zunubansu. 3 Saboda haka ina gab da cinye Ba'asha da gidansa, zan kuma
mai da gidanka kamar na Yerobowam ɗan Nebat. 4 Karnuka za su cinye waɗanda
suke na Ba'asha da suka mutu a birni, tsuntsaye kuma za su cinye waɗanda suka
mutu a jeji."
5 Game da sauran ayyukan mulkin Ba'asha, abin da ya yi, da kuma nasarorinsa,
an rubuta su cikin littafin tarihin sarakunan Isra'ila. 6 Ba'asha ya huta tare da
kakanninsa, aka kuma binne shi a Tirza. Sai Ela ɗansa ya gāje shi a matsayin sarki.
7 Ban da haka, maganar UBANGIJI ta zo ta wurin annabi Yehu ɗan Hanani wa
Ba'asha da gidansa, saboda dukan muguntar da ya aikata a gaban UBANGIJI, ya
tsokane shi yă yi fushi ta wurin abubuwan da ya yi, da kuma zama kamar gidan
Yerobowam, da kuma domin ya hallaka gidan Yerobowam.

### *Ela sarkin Isra'ila*

8 A shekara ta ashirin da shida ta Asa sarkin Yahuda, Ela ɗan Ba'asha ya zama
sarkin Isra'ila, ya kuma yi mulki a Tirza shekaru biyu.
9 Zimri, ɗaya daga cikin shugabanni, wanda ya shugabanci rabin kekunan yaƙin
Ela, ya yi maƙarƙashiya a kansa. Ela yana a Tirza a lokacin, ya bugu a gidan Arza,
sarkin fada a Tirza. 10 Zimri ya shiga, ya buge shi ya kashe a shekara ta ashirin da
bakwai na Asa sarkin Yahuda. Sa'an nan ya gāje shi a matsayin sarki.

11 Nan da nan sai ya fara mulki ya kuwa zauna a kujerar sarauta, ya kashe dukan
iyalin Ba'asha. Bai bar namiji guda ɗaya ba, ko dangi, ko aboki. 12 Ta haka Zimri ya
hallaka dukan iyalin Ba'asha, bisa ga maganar da Ubangiji ya yi game da Ba'asha ta
wurin annabi Yehu. 13 Wannan ya faru saboda dukan zunuban Ba'asha da waɗanda
ɗansa Ela ya yi, da ya sa Isra'ila suka yi, har suka tsokane Ubangiji, Allah na Isra'ila,
yă yi fushi ta wurin gumakansu marasa amfani.

14 Game da sauran ayyukan mulkin Ela, da dukan abin da ya yi, duk a rubuce suke
a cikin littafin tarihin sarakunan Isra'ila.

*Zimri sarkin Isra'ila*

15 A shekara ta ashirin da bakwai na Asa sarkin Yahuda, Zimri ya yi mulki a Tirza
kwana bakwai. Mayaƙa suka yi sansani kusa da Gibbeton, wani garin Filistiyawa.
16 Sa'ad da Isra'ilawa a cikin sansani suka ji cewa Zimri ya yi maƙarƙashiya a kan
sarki, ya kuma kashe shi, sai suka yi shela, suka naɗa Omri, shugaban mayaƙa ya
zama sarki a bisa Isra'ila, a wannan rana a cikin sansani. 17 Sai Omri da dukan
Isra'ilawa suka janye daga Gibbeton, suka yi wa Tirza kwanto. 18 Da Zimri ya ga
cewa an kame birnin, sai ya je ya shiga hasumiya fadan sarki ya sa wa fadan wuta
wutar kuwa ta ƙone shi ya mutu. 19 Wannan ya faru saboda zunuban da ya yi, ya yi
mugunta a gaban Ubangiji ya kuma yi tafiya a hanyoyin Yerobowam da kuma cikin
zunubin da Yerobowam ya yi da ya sa Isra'ila suka yi.

20 Game da sauran ayyukan mulkin Zimri, da tawayen da ya yi, duk a rubuce suke
a cikin littafin tarihin sarakunan Isra'ila.

*Omri sarkin Isra'ila*

21 Sai mutanen Isra'ila suka rabu kashi biyu; rabi guda sun goyi bayan Tibni ɗan
Ginat yă zama sarki, ɗayan rabin kuma sun goyi bayan Omri. 22 Amma mabiyan
Omri suka nuna sun fi na Tibni ɗan Ginat ƙarfi. Sai Tibni ya mutu, Omri kuwa ya
zama sarki.

23 A shekara ta talatin da ɗaya na Asa sarkin Yahuda, Omri ya zama sarkin Isra'ila,
ya kuma yi mulki shekara goma sha biyu, shekaru shida a Tirza. 24 Ya saya tudun
Samariya daga Shemer, a bakin talentin biyu na azurfa, ya kuma gina birni a kan
tudun, ya kira shi Samariya, bayan Shemer, sunan mai tudun a dā.

25 Amma Omri ya yi mugunta a gaban Ubangiji, ya kuma yi zunubi fiye da dukan
waɗanda suka kasance kafin shi. 26 Ya yi tafiya a dukan hanyoyin Yerobowam
ɗan Nebat da kuma cikin zunubinsa wanda ya sa Isra'ila suka yi, har suka tsokane
Ubangiji, Allah na Isra'ila yă yi fushi ta wurin gumakansu marasa amfani.

27 Game da sauran ayyukan mulkin Omri, abin da ya yi, da kuma abubuwan da
ya yi, duk a rubuce suke a cikin littafin tarihin sarakunan Isra'ila. 28 Omri ya huta
tare da kakanninsa, aka kuma binne shi a Samariya. Sai Ahab ya gāje shi a matsayin
sarki.

*Ahab ya zama sarkin Isra'ila*

29 A shekara ta talatin da takwas ta Asa sarkin Yahuda, Ahab ɗan Omri ya zama
sarkin Isra'ila, ya kuma yi mulki a Samariya a kan Isra'ila, shekara ashirin da biyu.
30 Ahab ɗan Omri ya yi mugunta sosai a gaban Ubangiji fiye da wani daga cikin
waɗanda suka riga shi. 31 Bai zama masa wani abu mai wuya ba, yă yi zunuban
Yerobowam ɗan Nebat, har ma ya auri Yezebel 'yar Etba'al sarkin Sidoniyawa, ya
kuma fara bauta wa Ba'al, ya yi masa sujada. 32 Ya kafa bagade domin Ba'al a
haikalin Ba'al da ya gina a Samariya. 33 Ahab ya gina ginshiƙin Ashera, ya kuma
aikata abubuwa masu yawa don yă tsokane Ubangiji, Allah na Isra'ila yă yi fushi fiye
da dukan sarakunan Isra'ila da suka riga shi.

34 A lokaci Ahab ne, Hiyel mutumin Betel ya sāke gina Yeriko. Ya kafa tushensa a
bakin ran ɗan farinsa Abiram, ya kuma kafa ƙofofinsa a bakin ran autansa Segub,
bisa ga maganar Ubangiji da ya yi ta wurin Yoshuwa ɗan Nun.

# 17

*Iliya ya sanar cewa za a yi babban fari*

1 To, Iliya mutumin Tishbe, daga Tishbe a Gileyad, ya ce wa Ahab, "Muddin
Ubangiji, Allah na Isra'ila wanda nake bauta wa yana a raye, ba za a yi raɓa ko
ruwan sama a 'yan shekaru masu zuwa ba, sai ko na faɗa haka."

*Hankaki sun ciyar da Iliya*

2 Sai maganar Ubangiji ta zo wa Iliya, ta ce, 3 "Ka bar nan, ka nufi wajajen gabas, ka
ɓuya a Rafin Kerit, gabas da Urdun. 4 Za ka sha daga rafin, zan kuma umarci hankaki
su ciyar da kai a can."
5 Saboda haka sai Iliya ya yi abin da Ubangiji ya faɗa masa. Ya tafi Rafin Kerit,
gabas da Urdun, ya zauna a can. 6 Hankaki suka riƙa kawo masa abinci da nama,
safe da yamma, ya kuma sha daga rafin.

*Gwauruwa a Zarefat*

7 Ana nan sai rafin ya bushe saboda ba a yi ruwan sama a ƙasar ba. 8 Sai maganar
Ubangiji ta zo wa Iliya cewa, 9 "Je ka, nan take, zuwa Zarefat na Sidon, ka zauna a
can. Na umarci wata gwauruwa a can tă ciyar da kai." 10 Saboda haka sai ya tafi
Zarefat. Sa'ad da ya isa ƙofar gari, sai ga wata gwauruwa tana tattara 'yan itace. Sai
ya kira ta, ya ce, "Ki kawo mini ɗan ruwa a tulu don in sha." 11 Da ta kama hanya
za tă tafi tă kawo, sai ya sāke kiranta ya ce, "Ina roƙonki, ki kuma kawo mini ɗan
abinci."
12 Sai ta ce masa, "Na rantse da Ubangiji Allahnka, ba ni da wani abinci, sai dai
ɗan gari hannu guda a tulu, da kuma ɗan mai a kwalaba. Ina tattara 'yan itacen nan
ne don in kai gida in yi abinci wa kaina da ɗana, don mu ci, mu mutu."
13 Iliya ya ce mata, "Kada ki ji tsoro. Ki tafi gida, ki yi yadda kika ce. Amma da
farko ki yi mini 'yar wainar burodi daga abin da kike da shi ki kawo mini, sa'an nan
ki yi wani abu wa kanki da kuma ɗanki. 14 Gama abin da Ubangiji, Allah na Isra'ila
ya ce, 'Tulun garin ba zai ƙare ba, kwalabar man kuma ba zai bushe ba sai ranar da
Ubangiji ya bayar da ruwan sama a ƙasar.' "
15 Sai ta tafi, ta yi yadda Iliya ya faɗa mata. Saboda haka aka kasance da abinci
kowace rana wa Iliya da kuma don macen da iyalinta. 16 Gama tulun garin bai ƙare
ba, kwalabar man kuma bai bushe ba, kamar yadda Ubangiji ya faɗa wa Iliya.
17 Ana nan sai ɗan matan, wato, gwauruwan nan ya fara ciwo. Ciwon ya ƙara
muni, daga ƙarshe sai ya daina numfashi. 18 Sai ta ce wa Iliya, "Mutumin Allah, yaya
haka? Ka zo ne domin ka nuna wa Allah zunubaina, ka kuma jawo mutuwar ɗana?"
19 Iliya ya ce, "Ki miƙa mini ɗanki." Sai ya ɗauke shi daga hannuwanta, ya kai
shi ɗakin sama inda yake zama, ya kwantar da shi a gadonsa. 20 Sa'an nan ya yi
kuka ga Ubangiji ya ce, "Ya Ubangiji Allahna, don me ka kawo wannan masifa a kan
gwauruwan nan? Kai ka ce in zauna tare da ita, ga shi yanzu ɗanta ya mutu." 21 Sai
ya kwanta, ya miƙe kansa a kan yaron sau uku, ya kuma yi kuka ga Ubangiji ya ce,
"Ya Ubangiji Allahna, ka mai da ran yaron nan!"
22 Ubangiji kuwa ya ji kukan Iliya, sai ran yaron ya dawo masa, ya kuma rayu.
23 Iliya ya ɗauki yaron ya sauko da shi daga ɗakin sama zuwa cikin gida. Ya ba da
shi ga mahaifiyarsa, ya ce, "Duba, ɗanki yana da rai!"
24 Sai matar ta ce wa Iliya, "Yanzu na san cewa kai mutumin Allah ne, Ubangiji
kuma yana magana ta wurinka."

# 18

## *Iliya da Obadiya*

1 Bayan dogon lokaci, a cikin shekara ta uku, maganar Ubangiji ta zo wa Iliya, ta ce,
“Tafi, ka gabatar da kanka ga Ahab, zan kuwa aika da ruwan sama a ƙasar.” 2 Saboda
haka Iliya ya tafi ya gabatar da kansa ga Ahab.

Yanzu dai yunwa ta tsananta a Samariya, 3 Ahab kuma ya aika a kawo Obadiya,
sarkin fadansa (Obadiya dai cikakken mai gaskata da Ubangiji ne. 4 Yayinda
Yezebel tana kisan annabawan Ubangiji, Obadiya ya ɗauki annabawa ɗari ya ɓoye
a kogwanni biyu, hamsin a kowanne, ya kuma tanada musu abinci da kuma ruwa.)
5 Ahab ya ce wa Obadiya, “Ka ratsa ƙasar zuwa dukan maɓulɓulai da fadamu. Mai
yiwuwa ka sami ciyawa mu ba dawakai da alfadarai don su rayu, don kada mu kashe
dabbobinmu.” 6 Saboda haka suka raba ƙasar da za su ratsa, Ahab zai tafi gefe ɗaya,
Obadiya kuma yă bi gefe ɗaya.

7 Yayinda Obadiya yana tafiya, sai Iliya ya sadu da shi. Obadiya ya gane shi, ya
rusuna har ƙasa, ya ce, “Kai ne, shugabana, Iliya?”

8 Iliya ya amsa, ya ce, “I, je ka faɗa wa maigidanka cewa, ‘Iliya yana a nan.’ ”

9 Obadiya ya yi tambaya, “Me na yi da ba daidai ba, da kake miƙa bawanka ga
Ahab don yă kashe? 10 Na rantse da Ubangiji Allahnka, babu al’umma ko masarauta
da mai girma sarki bai aika a nemo ka ba. In suka ce ba ka can, sai yă sa mulkin
ko al’ummar su rantse, cewa ai, ba su same ka ba. 11 Amma yanzu kana faɗa mini
in tafi wurin mai girma in ce, ‘Iliya yana a nan.’ 12 Ban san inda Ruhun Ubangiji zai
kai ka sa’ad da na bar ka ba. In na tafi na faɗa wa Ahab bai kuma same ka a nan
ba, zai sa a kashe ni. Tuna fa, ni bawanka, na yi wa Ubangiji sujada tun ina saurayi.
13 Ranka yă daɗe, ashe, ba a faɗa maka abin da na yi lokacin da Yezebel ta karkashe
annabawan Ubangiji ba? Yadda na ɓoye annabawa ɗari, na sa su hamsin-hamsin a
kogwanni biyu, na yi ta ba su abinci da ruwa. 14 Yanzu fa, kana ce in tafi wurin mai
girma sarki, in ce, ‘Iliya yana a nan.’ Ai, zai kashe ni!”

15 Iliya ya ce, “Na rantse da Ubangiji Maɗaukaki, wanda nake bauta wa, tabbatacce
zan gabatar da kaina ga Ahab a yau.”

## *Iliya a Dutsen Karmel*

16 Saboda haka sai Obadiya ya tafi wurin Ahab ya faɗa masa, Ahab kuwa ya tafi
wurin Iliya. 17 Sa’ad da Ahab ya ga Iliya, sai ya ce masa, “Kai ne wannan, kai mai
tā-da-na-zaune-tsaye a Isra’ila?”

18 Iliya ya amsa, ya ce, “Ban tā-da-na-zaune-tsaye a Isra’ila ba. Amma kai da iyalin
mahaifinka, ku kuka tā-da-na-zaune-tsaye. Ka ƙyale umarnai Ubangiji, ka bi Ba’al.
19 Yanzu ka tara mutane daga dukan Isra’ila su sadu da ni a kan Dutsen Karmel. Ka
kuma kawo annabawa ɗari huɗu da hamsin na Ba’al, da kuma annabawa ɗari huɗu
na Ashera, waɗanda suke ci a teburin Yezebel.”

20 Sai Ahab ya aika a duk fāɗin Isra’ila, ya kuma tattara annabawan a kan Dutsen
Karmel. 21 Iliya ya je gaban mutane ya ce, “Har yaushe za ku yi ta yawo tsakanin
ra’ayoyi biyu? In Ubangiji ne Allah, ku bi shi; amma in Ba’al Allah ne, ku bi shi.”

Mutane dai ba su ce uffam ba.

22 Sai Iliya ya ce musu, “Ni ne kaɗai annabin Ubangiji da ya rage, amma Ba’al yana
da annabawa ɗari huɗu da hamsin. 23 Ku samo mana bijimai biyu. Bari su zaɓa
ɗaya wa kansu, bari kuma su yanka shi kucu-kucu su sa a itace, sai dai, kada su sa
wuta a kansa. Ni kuwa zan shirya ɗaya bijimin in sa a kan itace, ni ma, ba zan sa
wuta a kansa ba. 24 Sa’an nan ku kira bisa sunan allahnku, ni kuwa zan kira bisa
sunan Ubangiji. Duk allahn da ya amsa ta wurin wuta, shi ne Allah.”

Sai dukan jama’a suka ce, “Abin nan da faɗa yana da kyau.”

25 Iliya ya ce wa annabawan Ba'al, "Ku ku fara zaɓi bijimi ɗaya, ku shirya, da yake
kuna da yawa. Ku kira a bisa sunan allahnku, amma kada ku ƙuna wuta." 26 Sai
suka ɗauki bijimin da aka ba su suka shirya shi.

Sa'an nan suka kira bisa sunan Ba'al daga safe har tsakar rana. Suna ihu, "Ya Ba'al,
ka amsa mana!" Amma babu wata amsa, babu wani da ya amsa. Suka yi ta rawa
kewaye da bagaden da suka yi.

27 Da tsakar rana, Iliya ya fara yin musu ba'a. Ya ce, "Ku yi ihu da ƙarfi, tabbatacce
shi allah ne! Mai yiwuwa yana cikin zurfin tunani, ko dai aiki ya yi masa yawa, ko ya
yi tafiya. Mai yiwuwa yana barci ne, dole a tashe shi." 28 Sai suka yi ta ihu da ƙarfi
suna tsattsaga kansu da takuba da māsu, yadda al'adarsu take, sai da jininsu ya yi ta
zuba. 29 Tsakar rana ta wuce, suka ci gaba da ƙoƙari, suna annabci har lokacin miƙa
hadayar yamma ya yi. Amma babu wani da ya tanƙa, babu wani da ya amsa, babu
wanda ya kula.

30 Sa'an nan Iliya ya ce wa dukan mutane, "Ku zo nan wurina." Suka zo wurinsa, ya
kuma shirya bagaden UBANGIJI, da ya riga ya zama kufai. 31 Iliya ya ɗauki duwatsu
goma sha biyu, ɗaya don kowace kabila zuriyar Yaƙub, wanda maganar UBANGIJI
ta zo masa, cewa, "Sunanka zai zama Isra'ila." 32 Da waɗannan duwatsun ya gina
bagade cikin sunan UBANGIJI, ya kuma haƙa wuriya kewaye da shi, isashe da zai ci
garwa biyu na irin ƙwayar gyada. 33 Ya shirya itace, ya yayyanka bijimin kucu-kucu,
ya shimfiɗa shi a itacen. Sa'an nan ya ce musu, "Ku cika manyan tuluna da ruwa,
ku zuba a kan hadayar da kuma a kan itacen." Suka zuba.

34 Ya ce, "Ku sāke yin haka," sai suka sāke yin haka.

Ya umarta, "Ku yi haka sau na uku," suka kuma yi haka sau na uku. 35 Ruwan ya
gangara kewaye da bagaden har ma ya cika wuriyar.

36 A lokacin hadaya, sai annabi Iliya ya zo gaba ya yi addu'a, ya ce, "Ya UBANGIJI
Allah na Ibrahim, na Isra'ila da kuma na Yaƙub, bari a sani a yau cewa kai Allah
ne a cikin Isra'ila, a kuma san cewa ni bawanka ne, na kuma yi dukan waɗannan
abubuwa bisa umarninka. 37 Ka amsa mini, ya UBANGIJI, ka amsa mini, saboda
waɗannan mutane su san cewa kai, ya UBANGIJI, kai ne Allah, su kuma san cewa
kana sāke juye zukatansu zuwa gare ka."

38 Sai wutar UBANGIJI ya fāɗo, ya cinye hadayar, itacen, duwatsun da kuma ƙasar,
ya lashe ruwan da yake cikin wuriyar.

39 Sa'ad da mutane suka ga wannan, sai suka rusuna, suka sunkuyar da kai suka
ce, "UBANGIJI, shi ne Allah! UBANGIJI, shi ne Allah!"

40 Sa'an nan Iliya ya umarce su, ya ce, "Ku kama annabawan Ba'al, kada ku bar
waninsu yǎ tsere!" Suka kama su, Iliya kuwa ya sa aka gangara da su zuwa Kwarin
Kishon, aka yayyanka su a can.

41 Sai Iliya ya ce wa Ahab, "Ka haura gida, ka ci, ka sha, gama ina jin motsin ruwan
sama mai yawa." 42 Sai Ahab ya ruga don yǎ ci, yǎ sha, amma Iliya ya hau kan
ƙwanƙolin Karmel, ya rusuna ƙasa, ya sa fuska a tsakanin gwiwarsa.

43 Ya ce wa bawansa, "Tafi ka dubi wajen teku." Sai bawan ya haura ya duba.

Ya ce, "Ba kome a can."

Sau bakwai Iliya ya ce, "Koma."

44 Sau na bakwai, bawan ya ce, "Wani girgije ƙarami kamar hannun mutum yana
tasowa daga teku."

Sai Iliya ya ce, "Je ka faɗa wa Ahab, 'Shirya keken yaƙinka, ka gangara kafin ruwan
sama yǎ tare ka.' "

45 Ana cikin haka, sarari ya ƙara duhunta da girgije, iska ta taso, sai ruwan sama
kamar da bakin kwarya ya sauko, Ahab kuwa ya hau zuwa Yezireyel. 46 Ikon UBANGIJI
ya sauko a kan Iliya, ya sha ɗamara, ya ruga a guje a gaban Ahab har zuwa Yezireyel.

# 19

*Iliya ya gudu zuwa Horeb*

1 Ahab fa ya faɗa wa Yezebel kome da Iliya ya yi, da yadda ya karkashe dukan
annabawan da takobi. 2 Saboda haka Yezebel ta aika da ɗan aika wa Iliya yă faɗa
masa, “Bari alloli su hukunta ni da tsanani, in war haka gobe ban mai da ranka
kamar na ɗaya daga cikin annabawan Ba’al ba.”
3 Iliya ya ji tsoro, ya gudu don yă ceci ransa. Sa’ad da ya kai Beyersheba a Yahuda,
sai ya bar bawansa a can. 4 Shi kuma ya yi tafiya yini guda zuwa cikin hamada. Ya
zo wurin wani itacen tsintsiya, ya zauna a ƙarƙashinsa, ya roƙa yă mutu. Ya ce, “Ya
ishe ni haka, Ubangiji, ka ɗauki raina; ban fi kakannina ba.” 5 Sa’an nan ya kwanta
a ƙarƙashin itacen ya yi barci.
Farat ɗaya sai wani mala’ika ya taɓa shi, ya ce, “Tashi ka ci abinci.” 6 Ya duba
kewaye, sai ga wainar burodi kusa da kansa a bisa garwashin wuta mai zafi, da
kuma tulun ruwa. Ya ci, ya sha, sa’an nan ya sāke kwanta.
7 Mala’ikan Ubangiji ya sāke dawowa sau na biyu ya taɓa shi, ya ce, “Tashi ka ci
abinci, gama tafiyar za tă yi maka yawa.” 8 Saboda haka ya tashi ya ci, ya kuma sha.
Ta wurin ƙarfin da ya samu saboda wannan abinci, ya yi tafiya yini arba’in da dare
arba’in, sai da ya kai Horeb, dutsen Allah. 9 A can ya shiga kogo ya kwana.

*Ubangiji ya bayyana wa Iliya*

Sai maganar Ubangiji ta zo masa, ta ce, “Me kake yi a nan, Iliya?”
10 Ya amsa, ya ce, “Ina kishi dominka Ubangiji, Allah Maɗaukaki. Isra’ilawa sun ƙi
alkawarinka, suka rurrushe bagadanka, suka kuma kashe annabawanka da takobi.
Ni ne kaɗai na rage, yanzu, ni ma suna ƙoƙari su kashe ni.”
11 Sai Ubangiji ya ce, “Fita ka tsaya a kan dutse a gaban Ubangiji, gama Ubangiji
yana shirin wucewa.”
Sai ga babbar iska mai ƙarfi ta tsage duwatsu, ta kuma ragargaza duwatsu a gaban
Ubangiji, amma Ubangiji ba ya cikin iskar. Bayan iskar sai aka yi girgizar ƙasa,
amma Ubangiji ba ya cikin girgizar ƙasa. 12 Bayan girgizar ƙasa, sai ga wuta, amma
Ubangiji ba ya cikin wuta. Bayan wutar kuma sai ga wata ’yar murya. 13 Sa’ad da
Iliya ya ji ta, ya ja mayafinsa ya rufe fuskarsa, ya fita ya tsaya a bakin kogon.
Sai ya ji murya ta ce masa, “Me kake yi a nan, Iliya?”
14 Ya amsa, ya ce, “Ina kishi dominka Ubangiji, Allah Maɗaukaki. Isra’ilawa sun ƙi
alkawarinka, suka rurrushe bagadanka, suka kuma kashe annabawanka da takobi.
Ni ne kaɗai na rage, yanzu, ni ma suna ƙoƙari su kashe ni.”
15 Sai Ubangiji ya ce masa, “Ka koma ta hanyar da ka zo, ka tafi Hamadan
Damaskus. Sa’ad da ka kai can, ka shafe Hazayel yă zama sarki bisa Aram. 16 Ka
kuma shafe Yehu ɗan Nimshi yă zama sarkin Isra’ila, ka shafe Elisha ɗan Shafat
daga Abel-Mehola yă gāje ka a matsayin annabi. 17 Yehu zai kashe duk wani wanda
ya tsere wa takobin Hazayel, Elisha kuwa zai kashe duk wani wanda ya tsere wa
takobin Yehu. 18 Duk da haka zan bar mutane dubu bakwai na Isra’ila waɗanda ba
su rusuna da gwiwansu wa Ba’al ba, ba su kuma sumbace shi da bakinsu ba.”

*Kiran Elisha*

19 Sai Iliya ya tafi daga can ya sami Elisha ɗan Shafat, yana noma da shanu goma
sha biyu masu garman noma, shi kansa yana jan na goma sha biyun. Iliya ya tafi
wurinsa ya jefa mayafinsa a kan Elisha. 20 Sai Elisha ya bar shanun, ya ruga ya bi
Iliya. Ya ce, “Bari in sumbace mahaifina da mahaifiyata, in yi musu bankwana, sa’an
nan in zo in bi ka.”
Iliya ya ce, “Koma! Me na yi maka?”

[21] Sai Elisha ya bar shi, ya koma, ya ɗauki shanunsa ya yayyanka. Ya ƙone kayan
garman noman don yǎ dafa naman, ya kuma ba wa mutane naman, suka kuwa ci.
Sa'an nan ya tashi, ya bi Iliya, ya kuma zama mai hidimarsa.

# 20

*Ben-Hadad ya yaƙi Samariya*

[1] Ben-Hadad sarkin Aram kuwa ya tattara mayaƙansa gaba ɗaya. Sarakuna talatin
da biyu suka tafi tare da shi haɗe da dawakansu da kekunan yaƙinsu. Ya haura ya
yi wa Samariya kwanto, ya kuma yaƙe ta. [2] Ya aika da 'yan aika zuwa cikin birnin
wurin Ahab sarkin Isra'ila yana cewa, "Ga abin da Ben-Hadad ya ce, [3] 'Azurfarka da
zinariyarka nawa ne. Mafi kyau cikin matanka da 'ya'yanka nawa ne.' "
[4] Sarkin Isra'ila ya amsa, ya ce, "Kamar dai yadda ka faɗa, ranka yǎ daɗe, sarki.
Ni da dukan abin da nake da shi, naka ne."
[5] Sai 'yan aikan suka sāke dawo suka ce, "Ga abin da Ben-Hadad ya ce, 'Na aika
ka ba da azurfarka da zinariyarka, matanka da kuma 'ya'yanka. [6] Amma war haka
gobe zan aika shugabannina su bincika fadanka da kuma gidajen shugabanninka. Za
su kwashe dukan abubuwan da kake ganin darajarsu su tafi.' "
[7] Sarkin Isra'ila ya tattara dukan dattawan ƙasar, ya ce musu, "Ku duba fa, wannan
mutum yana neman tsokana! Sa'ad da ya aika in ba shi matana da 'ya'yana, azurfana
da zinariyana, ban hana masa ba."
[8] Dattawa da dukan mutane suka amsa, suka ce, "Kada ka saurare shi ko ka yarda
da abin da yake bukata."
[9] Saboda haka ya ba wa 'yan aikan Ben-Hadad amsa, ya ce, "Ku faɗa wa ranka yǎ
daɗe, sarki, 'Bawanka zai yi dukan abin da ka bukaci da farko, amma wannan na
ƙarshe ba zan iya yin ba.' " Suka tafi suka kai amsar wa Ben-Hadad.
[10] Sai Ben-Hadad ya aika da wani saƙo wa Ahab, ya ce, "Bari alloli su yi da ni yadda
suke so, su kuma yi haka da tsanani, in isashen ƙura ta rage a Samariya da za a iya
ba wa mutanena a tafin hannu."
[11] Sarki Isra'ila ya amsa, ya ce, "Ku faɗa masa, 'Wanda ya sa kayan yaƙinsa bai
kamata yǎ yi fariya ba sai ya tuɓe su.' "
[12] Ben-Hadad ya ji wannan saƙo yayinda shi da sarakunan suke sha a cikin
tentunansu, sai ya umarce mutanensa, ya ce, "Ku shirya don yaƙi." Saboda haka
suka shirya don su yaƙi birnin.

*Ahab ya ci Ben-Hadad da yaƙi*

[13] Ana cikin haka sai wani annabi ya zo wurin Ahab sarkin Isra'ila ya sanar masa
cewa, "Ga abin da UBANGIJI ya ce, 'Ka ga wannan ɗumbun mayaƙa? Zan ba da su
cikin hannunka a yau, sa'an nan za ka san cewa ni ne UBANGIJI.' "
[14] Ahab ya ce, "Amma wa zai yi haka?"
Annabin ya amsa, "Ga abin da UBANGIJI ya ce, 'Sojoji matasa na shugabannin
yankuna za su yi haka.' "
Ya tambaya, "Wa kuma zai fara yaƙin?"
Annabin ya amsa, "Kai za ka fara."
[15] Saboda haka Ahab ya kira sojoji matasa na shugabannin yankuna, mutum 232.
Sa'an nan ya tattara sauran Isra'ilawa su 7,000 gaba ɗaya. [16] Suka fita da tsakar rana
yayinda Ben-Hadad tare da sarakuna 32 masu goyon bayansa suke cikin tentunansu
suna sha, suna buguwa. [17] Sojojin nan matasa na shugabannin yankuna suka fara
fita.
Ben-Hadad kuwa ya riga ya aiki 'yan leƙen asiri, waɗanda suka ce, "Mutane suna
zuwa daga Samariya."

18 Ya ce, "In sun fito don salama, ku kamo su da rai; in sun fito yaƙi ne, ku kamo su da rai."
19 Sojojin nan matasa na shugabannin yankuna suka taka suka fita daga birnin da
mayaƙa a bayansu. 20 Kowannensu kuwa ya buge abokin gābansa. Ganin wannan,
sai Arameyawa suka gudu, Isra'ilawa suna bi. Amma Ben-Hadad na Aram ya tsere a
kan dokinsa tare da waɗansu mahayan dawakansa. 21 Sarki Isra'ila ya bi, ya kuma
sha ƙarfin dawakan da keken yaƙin, ya kashe Arameyawa da yawa.
22 Daga baya, annabin ya zo wurin sarkin Isra'ila ya ce, "Ka ƙarfafa matsayinka ka kuma ga abin da za a yi, gama a bazara mai zuwa sarkin Aram zai sāke kawo yaƙi."
23 Ana cikin haka, shugabannin sarkin Aram suka ba shi shawara, "Allolinsu, allolin
tuddai ne. Shi ya sa suka fi mu ƙarfi. Amma in mun yaƙe su a fili, tabbatacce za mu
fi su ƙarfi. 24 Ka yi wannan. Ka cire dukan sarakuna daga matsayinsu ka sa waɗansu
shugabanni a maimakonsu. 25 Dole kuma ka tā da waɗansu mayaƙa kamar waɗanda
ka rasa, doki don doki, keken yaƙi kuma don keken yaƙi, saboda mu iya yaƙe Isra'ila
a fili. Ta haka tabbatacce za mu fi ƙarfinsu." Sai ya yarda da su, ya kuma yi haka.
26 Bazara na biye Ben-Hadad ya tattara Arameyawa, ya haura zuwa Afek don yă
yaƙi Isra'ila. 27 Sa'ad da aka tattara Isra'ilawa, aka kuma ba su guzuri, sai suka taka
suka fita don su sadu da Arameyawa. Isra'ilawa suka kafa sansani ɗaura da su kamar
ƙananan garkuna biyu na awaki, yayinda Arameyawa suka rufe dukan jejin.
28 Sai mutumin Allah ya zo ya ce wa sarkin Isra'ila, "Ga abin da UBANGIJI ya ce, 'Domin Arameyawa suna tsammani UBANGIJI allahn tuddai ne, ba allahn kwari ba, zan ba da wannan ɗumbun mayaƙa a hannuwanka, za ka kuwa sani ni ne UBANGIJI.' "
29 Kwana bakwai suka yi sansani ɗaura da juna, a rana ta bakwai sai yaƙi ya haɗu.
Isra'ilawa suka kashe sojojin kafa na Arameyawa dubu ɗari a rana ɗaya. 30 Sauransu
suka tsere zuwa birnin Afek, inda katangar ya fāɗa a kan mutum dubu ashirin da
bakwai. Sai Ben-Hadad ya gudu zuwa birni ya ɓuya a ciki cikin ɗaki.
31 Fadawansa suka je suka ce masa, "Mun ji an ce sarakunan Isra'ila masu jinƙai ne, bari mu sa tufafin makoki, mu ɗaura igiyoyi a wuyanmu, sa'an nan mu tafi wurin sarkin Isra'ila, wataƙila zai bar ka da rai."
32 Saye da tufafin makoki kewaye a gindinsu, da kuma igiyoyi kewaye da kawunansu, suka tafi wurin sarkin Isra'ila, suka ce, "Bawanka Ben-Hadad ya ce, 'Ina roƙonka bari in rayu.' "

Sarki ya amsa, "Har yanzu yana da rai? Shi ɗan'uwana ne."

33 Da ma abin da fadawan suke so su ji ke nan, sai suka yi sauri, suka karɓi maganar a bakinsa, suka ce, "I, ɗan'uwanka, Ben-hadad!"

Sarki ya ce, "Ku je ku kawo shi." Da Ben-Hadad ya fita, sai Ahab ya sa aka kawo shi cikin keken yaƙinsa.

34 Ben-Hadad ya ce, "Zan mayar da biranen mahaifinka da na ƙwace daga mahaifinka. Za ka iya sa wurin kasuwarka a cikin Damaskus, kamar yadda mahaifinka ya yi a Samariya."

Ahab ya ce, "Bisa wannan yarjejjeniya zan sake ka." Saboda haka ya yi yarjejjeniya da shi, sai ya bar shi ya tafi.

### *Annabi ya yi wa Ahab Allah wadai*

35 Ta wurin maganar UBANGIJI, ɗaya daga cikin 'ya'ya maza na annabawa ya ce wa abokinsa, "Ka buge ni da makaminka," amma mutumin ya ƙi.
36 Sai annabin ya ce, "Domin ba ka yi biyayya da UBANGIJI ba, da zarar ka bar ni zaki zai kashe ka." Daga baya mutumin ya tafi, zaki ya same shi, ya kuma kashe shi.
37 Annabin ya sami wani mutum ya ce, "Ka buge ni, ina roƙonka." Sai mutumin
ya buge shi, ya ji masa ciwo. 38 Sa'an nan annabin ya tafi ya tsaya a bakin hanya
yana jiran sarki. Ya ɓad da kamanni da ƙyalle a kansa. Kyallen ya sauka zuwa bisa

idanunsa. 39 Yayinda sarki yake wucewa, sai annabin ya yi kira da ƙarfi gare shi
ya ce "Ni bawanka na tafi yaƙi, sai ga wani ya kawo mini wani mutum, ya ce, 'Ka
riƙe wannan mutum, kada ka bar shi yă kuɓuta ko da ƙaƙa, idan ka bari ya kuɓuta,
a bakin ranka, ko kuwa ka biya talanti ɗaya na azurfa.' 40 Yayinda bawanka yana
fama, yana kai da kawowa, sai mutumin ya ɓace."

Sai sarkin Isra'ila ya ce, "Hukuncinka ke nan, ka furta shi da kanka."

41 Sai annabin ya cire ƙyallen da sauri daga kansa, da ya rufe idanunsa, sarkin
Isra'ila kuwa ya gane shi a matsayi ɗaya daga cikin annabawa. 42 Sai ya ce wa sarki,
"Ga abin da UBANGIJI ya ce, 'Ka saki mutumin da na ƙudura yă mutu. Saboda haka
ranka zai zama a maimakon ransa, mutanenka a maimakon mutanensa.' " 43 Cike da
fushi, sarkin Isra'ila ya tafi fadarsa a Samariya.

# 21

*Gonar inabin Nabot*

1 Ana nan bayan haka sai waɗannan abubuwa suka faru. Nabot mutumin Yezireyel
yana da gonar inabi a Yezireyel, a yankin Samariya, kusa da gidan Sarki Ahab. 2 Sai
Ahab ya ce wa Nabot, "Ka ba ni gonar inabinka in yi amfani da ita don kayan lambu,
da yake tana kusa da fadana. Zan ba ka wata gonar inabin da ta fi wannan, ko kuma
in ka gwammace, sai in biya ka duk abin da ya dace da ita."

3 Amma Nabot ya amsa wa Ahab ya ce, "UBANGIJI yă sawwaƙe in ba ka gādon
kakannina."

4 Ahab ya cika da fushi saboda Nabot, mutumin Yezireyel ya ce, "Ba zan ba ka
gādon kakannina ba." Ya kwanta a gadonsa yana zub da hawaye, ya kuma ƙi cin
abinci.

5 Matarsa Yezebel ta shiga ciki ta tambaye shi, ta ce, "Me ya sa ka kumbura? Me ya
sa ba za ka ci abinci ba?"

6 Sai ya amsa mata, ya ce, "Domin na ce wa Nabot mutumin Yezireyel, 'Ka sayar
mini gonar inabinka; ko kuwa in ka gwammace, zan ba ka wata gonar inabi a
maimakonta.' Amma ya ce, 'Ba zan ba ka gonar inabina ba.' "

7 Yezebel matarsa ta ce, "Yaya kake yi kamar ba kai ne sarki Isra'ila ba? Tashi ka
ci abinci! Ka yi farin ciki. Zan ba ka gonar inabin Nabot mutumin Yezireyel."

8 Sai ta rubuta wasiƙu a sunan Ahab, ta buga hatiminsa a kansu, sa'an nan ta aika
su ga dattawa da manyan gari waɗanda suke zama a birnin da Nabot yake. 9 Cikin
waɗannan wasiƙu ta rubuta,

"Ku yi shelar ranar azumi, ku zaunar da Nabot a wuri mai martaba a cikin
mutane. 10 Amma ku zaunar da waɗansu 'yan iska biyu ɗaura da shi, ku sa su
ba da shaida cewa ya zagi Allah da sarki. Sa'an nan ku ɗauke shi ku jajjefe shi da
dutse sai ya mutu."

11 Sai dattawa da manyan gari, waɗanda suke zama a birnin da Nabot yake, suka
yi kamar yadda Yezebel ta umarta a cikin wasiƙun da ta rubuta. 12 Suka yi shelar
azumi, suka kuma zaunar da Nabot a wuri mai martaba a cikin mutane. 13 Sa'an
nan 'yan iska biyu suka zo, suka zauna ɗaura da shi, suka kawo zarge a kan Nabot
a gaban mutane, suna cewa, "Nabot ya zagi Allah da sarki." Saboda haka aka ɗauke
shi waje da birnin, aka jajjefe shi da dutse har ya mutu. 14 Sa'an nan suka aika wa
Yezebel. "An jajjefe Nabot, ya kuma mutu."

15 Nan da nan sa'ad da Yezebel ta ji cewa an jajjefe Nabot da dutse ya kuma mutu,
sai ta ce wa Ahab, "Tashi ka mallaki gonar inabin Nabot mutumin Yezireyel wanda
ya ƙi ya sayar maka. Ba shi da rai, ya mutu." 16 Da Ahab ya ji cewa Nabot ya mutu,
sai ya tashi ya gangara don yă mallaki gonar inabin Nabot.

17 Sai maganar UBANGIJI ta zo wa Iliya mutumin Tishbe. 18 Ta ce, “Gangara don
ka sadu da Ahab sarkin Isra’ila, wanda yake mulki a Samariya. Yanzu yana a gonar
inabin Nabot, inda ya tafi yǎ mallake ta. 19 Ka ce masa, Ga abin da UBANGIJI ya ce,
‘Ba ka kashe mutum ka kuma ƙwace kayansa ba?’ Sa’an nan ka ce masa ga abin da
UBANGIJI ya ce, ‘A inda karnuka suka lashe jinin Nabot, karnuka za su lashe jininka,
I, naka!’ ”

20 Ahab ya ce wa Iliya, “Wato, ka same ni kuma, abokin gābana!”

Sai ya amsa ya ce, “Na same ka, domin ka sayar da kanka ga yin mugunta a gaban
UBANGIJI. 21 ‘Zan kawo masifa a kanka. Zan kawar da zuriyarka, in kuma yanke
daga Ahab kowane ɗa namiji na ƙarshe cikin Isra’ila, bawa ko ’yantacce. 22 Zan mai
da gidanka kamar gida Yerobowam ɗan Nebat, da na Ba’asha ɗan Ahiya, domin ka
tsokane ni har na yi fushi, ka kuma sa Isra’ila ya yi zunubi.’

23 “Game da Yezebel kuwa UBANGIJI ya ce, ‘Karnuka za su cinye Yezebel a katangar
Yezireyel.’

24 “Karnuka za su cinye waɗanda suke na Ahab waɗanda suka mutu a cikin birni,
tsuntsayen sararin sama kuma za su cinye waɗanda suka mutu a jeji.”

25 (Babu wani mutum kamar Ahab, wanda ya ba da kansa ga aikata mugunta a
gaban UBANGIJI. Yezebel matarsa ce ta zuga shi. 26 Ya yi abar ƙyama ƙwarai ta wurin
bin gumaka, kamar Amoriyawan da UBANGIJI ya kora a gaban Isra’ila.)

27 Sa’ad da Ahab ya ji waɗannan kalmomi, sai ya yage rigarsa, ya sa rigunan
makoki, ya kuma yi azumi. Ya kwanta a kayan makoki, ya kuma yi tafiya cikin
sauƙinkai.

28 Sai maganar UBANGIJI ta zo wa Iliya mutumin Tishbe, ta ce, 29 “Ka lura da yadda
Ahab ya ƙasƙantar da kansa a gabana kuwa? Domin ya ƙasƙantar da kansa, ba zan
kawo wannan masifa a kwanakinsa ba, amma zan kawo ta a kan gidansa a kwanakin
ɗansa.”

# 22

*Mikahiya ya yi annabci a kan Ahab*
*(2 Tarihi 18.2-27)*

1 Aka yi shekaru uku ba a yi yaƙi tsakanin Aram da Isra’ila ba. 2 Amma a shekara
ta uku, Yehoshafat sarkin Yahuda ya gangara don yǎ ga sarki Isra’ila. 3 Sarkin Isra’ila
ya ce wa shugabanninsa, “Ba ku san cewa Ramot Gileyad namu ne ba, duk da haka
ba mu yi kome ba don mu sāke karɓanta daga sarkin Aram?”

4 Saboda haka ya tambayi Yehoshafat, ya ce, “Za ka tafi tare da ni don in yi yaƙi da
Ramot Gileyad?”

Yehoshafat ya amsa wa sarkin Isra’ila, ya ce, “Ni ma kamar ka ne, mutanena kuwa
kamar mutanenka, dawakaina kamar dawakanka.” 5 Amma Yehoshafat ya ce wa
sarkin Isra’ila, “Da farko mu nemi nufin UBANGIJI.”

6 Saboda haka sarkin Isra’ila ya tattara annabawa, kamar ɗari huɗu, ya tambaye
su, “In kai yaƙi a kan Ramot Gileyad, ko kada in kai?”

Suka amsa, “Ka tafi, gama Ubangiji zai ba ka ita a hannunka.”

7 Amma Yehoshafat ya yi tambaya, ya ce, “Babu wani annabin UBANGIJI a nan da
za mu tambaya?”

8 Sarkin Isra’ila ya amsa wa Yehoshafat, ya ce, “Akwai mutum guda har yanzu
wanda ta wurinsa za mu iya nemi nufin UBANGIJI, amma na ƙi jininsa domin bai
taɓa yin annabci wani abu mai kyau game da ni ba, sai dai mummuna kullum. Shi
ne Mikahiya ɗan Imla.”

Yehoshafat ya ce, “Kada sarki ya ce haka.”

9 Saboda haka sarkin Isra’ila ya kira ɗaya daga cikin shugabanninsa ya ce, “Kawo
Mikahiya ɗan Imla nan take.”

10 Saye da rigunansu na sarauta, sarkin Isra’ila da Yehoshafat sarkin Yahuda suna
zama a kujerun sarautarsu a masussuka ta mashigin ƙofar Samariya, tare da dukan
annabawa suna ta annabci a gabansu. 11 Zedekiya ɗan Kena’ana kuwa ya yi ƙahonin
ƙarfe ya kuma furta, “Ga abin da Ubangiji ya ce, ‘Da waɗannan za ka tunkuyi
Arameyawa har su hallaka.’ ”

12 Dukan sauran annabawan suka yi annabci iri abu ɗaya. Suka ce, “Ka yaƙi Ramot
Gileyad, ka kuma yi nasara, gama Ubangiji zai ba da ita cikin hannun sarki.”

13 Ɗan aikan da ya je yă kawo Mikahiya, ya ce masa, “Duba, sauran annabawa
suna maganar nasara wa sarki, sai ka ce mutum guda. Bari maganarka tă yarda da
tasu, ka kuma yi maganar alheri.”

14 Amma Mikahiya ya ce, “Na rantse da Ubangiji mai rai, zan faɗa masa kawai abin
da Ubangiji ya faɗa mini.”

15 Da suka kai, sai sarki ya tambaye shi, ya ce, “Mikahiya, mu kai yaƙi a kan Ramot
Gileyad, ko kada mu kai?”

Ya amsa ya ce, “Yaƙe ta, za ka kuwa yi nasara, gama Ubangiji zai ba da ita cikin
hannun sarki.”

16 Sai sarki ya ce masa, “Sau nawa ne zan sa ka rantse cewa ba za ka faɗa mini
kome ba sai dai gaskiya a cikin sunan Ubangiji?”

17 Sa’an nan Mikahiya ya amsa, “Na ga dukan Isra’ila a warwatse a kan tuddai
kamar tumakin da ba su da makiyayi, kuma Ubangiji ya ce, ‘Waɗannan mutane ba
su da maigida. Bari kowa yă tafi gida cikin salama.’ ”

18 Sai sarkin Isra’ila ya ce wa Yehoshafat, “Ban faɗa maka cewa bai taɓa yin annabci
wani abu mai kyau game da ni, sai mummuna kawai ba?”

19 Mikahiya ya ci gaba, “Saboda haka ka ji maganar Ubangiji. I, na ga Ubangiji
zaune a kursiyinsa tare da dukan rundunar sama tsaye kewaye da shi a dama da
hagunsa. 20 Kuma Ubangiji ya ce, ‘Wa zai ruɗi Ahab zuwa yaƙi da Ramot Gileyad, yă
kuma kai shi mutuwarsa a can?’

“Wani ya ce wannan, wani ya ce wancan. 21 A ƙarshe, wani ruhu ya zo gaba, ya
tsaya a gaban Ubangiji ya ce, ‘Zan ruɗe shi.’

22 “Ubangiji ya yi tambaya ‘Ta wace hanya?’ Ya ce,

“ ‘Zan tafi in zama ruhun ƙarya a bakunan dukan annabawansa.’

“Ubangiji ya ce, ‘Za ka yi nasara a ruɗinsa. Ka tafi, ka yi haka.’

23 “Saboda haka yanzu Ubangiji ya sa ruhun ƙarya a bakunan dukan annabawanka.
Ubangiji ya zartar maka da masifa.”

24 Sai Zedekiya ɗan Kena’ana ya hau ya mari Mikahiya a fuska. Ya yi tambaya, “A
wace hanya ce ruhu daga Ubangiji ya bar ni ya yi maka magana?”

25 Mikahiya ya amsa, “Za ka gane a ranar da ka je ka ɓuya a ciki cikin ɗaki.”

26 Sa’an nan sarkin Isra’ila ya umarta, “Ku kama Mikahiya, ku kai shi wurin Amon,
shugaban birnin, da wurin Yowash ɗan sarki. 27 Ku ce ga abin da sarki ya ce, ‘Ku sa
wannan mutum a kurkuku, kuma kada ku ba shi wani abu sai dai burodi da ruwa,
sai na dawo lafiya.’ ”

28 Mikahiya ya furta, “Idan har ka dawo lafiya, to, Ubangiji bai yi magana ta wurina
ba.” Ya kuma ƙara da cewa, “Ku lura da maganata, dukanku mutane!”

### *An kashe Ahab a Ramot Gileyad*
### *(2 Tarihi 18.28-34)*

29 Sai sarkin Isra’ila da Yehoshafat sarkin Yahuda suka haura zuwa Ramot Gileyad.
30 Sarkin Isra’ila ya ce wa Yehoshafat, “Zan ɓad da kama in shiga wurin yaƙi, amma

ka sa kayan sarautarka.” Saboda haka sarkin Isra’ila ya ɓad da kama, ya shiga cikin yaƙi.
31 Sarkin Aram kuwa ya umarci shugabanni kekunan yaƙinsa talatin da biyu,
ya ce, “Kada ku yaƙe kowa, ƙarami ko babba, sai dai sarkin Isra’ila.” 32 Sa’ad
da shugabannin kekunan yaƙin suka ga Yehoshafat, suka yi tsammani, suka ce,
“Tabbatacce wannan shi ne sarkin Isra’ila.” Saboda haka suka juye don su yaƙe
shi, amma sa’ad da Yehoshafat ya yi ihu, 33 sai shugabannin kekunan yaƙin suka ga
ashe ba sarkin Isra’ila ba ne, sai suka daina binsa.
34 Amma wani ya ja bakansa kawai ya bugi Ahab sarkin Isra’ila a tsakanin sassan
kayan yaƙinsa. Sai sarki ya ce wa mahayin keken yaƙinsa, “Juye, ka fitar da ni daga
yaƙin. An ji mini rauni.” 35 Dukan yini aka yi ta yaƙi, aka kuma riƙe sarki a keken
yaƙinsa yana fuskanci Arameyawa. Jini daga mikinsa ya yi ta zuba a ƙasan keken
yaƙin, a wannan yamma kuwa ya mutu. 36 Da rana tana fāɗuwa, sai kuka ta bazu
cikin mayaƙa, “Kowane mutum ya tafi garinsu; kowa ya tafi ƙasarsa!”
37 Sai sarki ya mutu, aka kuwa kawo shi Samariya, aka binne shi a can. 38 Suka
wanke keken yaƙi a tafki, a Samariya (inda karuwai suke wanka), sai karnuka suka
lashe jininsa, kamar yadda maganar Ubangiji ta furta.
39 Game da sauran ayyukan mulkin Ahab, haɗe da dukan abin da ya yi, da fadan da
ya gina ya kuma shimfiɗa da hauren giwa, da biranen da ya gina, duk a rubuce suke
a cikin littafin tarihin sarakunan Isra’ila. 40 Ahab ya huta da kakanninsa. Ahaziya
ɗansa ya gāje shi a matsayin sarki.

### *Yehoshafat sarkin Yahuda*
### *(2 Tarihi 20.31–21.1)*

41 Yehoshafat ɗan Asa ya zama sarkin Yahuda a shekara ta huɗu ta Ahab sarkin
Isra’ila. 42 Yehoshafat yana da shekara talatin da biyar sa’ad da ya zama sarki, ya
kuma yi mulki a Urushalima shekaru ashirin da biyar. Sunan mahaifiyarsa, Azuba
’yar Shilhi. 43 A cikin kome ya yi tafiya a hanyoyin mahaifinsa Asa, bai kuma kauce
daga gare su ba; ya yi abin da yake daidai a gaban Ubangiji. Amma bai rurrushe
masujadai da suke kan tuddai ba, mutane kuwa suka ci gaba da miƙa hadayu suna
kuma ƙone turare a can. 44 Yehoshafat kuma ya zauna lafiya da sarkin Isra’ila.
45 Game da sauran ayyukan mulkin Yehoshafat da abubuwan da ya yi, da kuma
yaƙe-yaƙensa, duk a rubuce suke a cikin littafin tarihin sarakunan Yahuda. 46 Ya
kawar da karuwai maza na masujadai da suke kan tuddai waɗanda suka rage tun
mulkin mahaifinsa Asa. 47 Babu sarki a lokacin Edom, saboda haka sai mataimaki ya
yi mulki.
48 To, Yehoshafat ya gina jerin jiragen ruwan kasuwanci* don su je Ofir saboda
zinariya, amma ba su yi tafiya ba, gama sun farfashe a Eziyon Geber. 49 A lokacin
Ahaziya ɗan Ahab ya ce wa Yehoshafat, “Bari mutanena su tafi tare da mutanenka,”
amma Yehoshafat ya ƙi.
50 Yehoshafat kuwa ya huta tare da kakanninsa, aka kuma binne shi tare da su a
birnin Dawuda kakansa. Sai Yehoram ɗansa ya gāje shi.

### *Ahaziya sarkin Isra’ila*

51 Ahaziya ɗan Ahab ya zama sarkin Isra’ila a Samariya a shekara ta goma sha
bakwai ta Yehoshafat sarkin Yahuda, ya kuma yi mulki a bisa Isra’ila shekaru biyu.
52 Ya aikata mugunta a gaban Ubangiji, domin ya yi tafiya a hanyoyin mahaifinsa da
na mahaifiyarsa, da kuma a hanyoyin Yerobowam ɗan Nebat, wanda ya sa Isra’ila
suka yi zunubi. 53 Ya bauta, ya kuma yi wa Ba’al sujada, ya tsokane Ubangiji, Allah
na Isra’ila yă yi fushi, kamar yadda mahaifinsa ya yi.

* **22:48** Da Ibraniyanci na jiragen Tarshish

# 2 Sarakuna

1 Bayan mutuwar Ahab, Mowab ta yi wa Isra'ila tawaye. 2 Ahaziya fa ya fāɗo daga
tagar ɗakin samansa a Samariya ya ji rauni. Saboda haka ya aiki masinjoji, yana
cewa, "Ku je ku tuntuɓi Ba'al-Zebub, allahn Ekron, ku ga ko zan warke daga wannan
rauni."
3 Amma mala'ikan UBANGIJI ya ce wa Iliya mutumin Tishbe, "Ka haura ka taryi
masinjojin sarkin Samariya, ka tambaye su, 'Don babu Allah ne a Isra'ila da za ku
tafi ku tuntuɓi Ba'al-Zebub allahn Ekron?' 4 Saboda haka, ga abin da UBANGIJI ya ce,
'Ba za ka tashi daga inda kake kwance ba, ba shakka za ka mutu!' "

Iliya ya yi kamar yadda Ubangiji ya umarce shi, sai ya tafi.

5 Da masinjojin suka koma wurin sarki, sai sarki ya ce da su, "Don me kuka komo?"

6 Sai suka amsa, "Wani mutum ya sadu da mu ya ce mana, 'Ku koma wurin sarkin
da ya aike ku, ku ce masa, "Ga abin da UBANGIJI ya ce, don babu Allah ne a Isra'ila da
ka aika a tuntuɓi Ba'al-Zebub allahn Ekron? Saboda haka ba za ka tashi daga gadon
da kake kwance ba. Ba shakka za ka mutu!" ' "
7 Sai Sarkin ya tambaye su ya ce, "Wanda irin mutum ne ya yi muku wannan
magana?"

8 Sai suka ce, "Mutumin ya sa riga mai gashi, ya kuma yi ɗamara da fata."

Sarkin ya ce, "Ai, Iliya mutumin Tishbe nan ne."

9 Sai sarki ya aiki kaftin da sojojin hamsin wurin Iliya. Kaftin ya haura wajen Iliya,
wanda yake zaune a kan tudu, ya ce masa, "Mutumin Allah, sarki ya ce, 'Ka sauko,
ka zo!' "
10 Iliya ya ce masa, "In ni mutumin Allah ne, bari wuta tă sauko daga sama tă cinye
ka da sojojinka hamsin!" Sai wuta ta sauko daga sama ta cinye kaftin tare da sojojinsa
hamsin.
11 Da jin haka sai sarki ya sāke aiken wani kaftin tare da waɗansu sojojinsa hamsin
wurin Iliya. Kaftin ya ce wa Iliya, "Mutumin Allah, ga abin da sarki ya ce, 'Ka sauko,
nan take ka zo!' "
12 Sai Iliya ya amsa, "In ni mutumin Allah ne, bari wuta ta sauko daga sama ta
cinye ka da sojojinka hamsin!" Sai wutar Allah ta sauko daga sama ta cinye shi da
sojojinsa hamsin.
13 Saboda haka sai sarki ya aiki kaftin na uku da sojojinsa hamsin. Wannan kaftin
na ukun ya haura ya durƙusa a gaban Iliya, ya roƙe shi ya ce, "Mutumin Allah, ina
roƙonka ka dubi darajar raina da na waɗannan sojoji hamsin, bayinka! 14 Duba,
wuta ta sauko daga sama ta cinye su kaftin nan biyu waɗanda suka zo da farko da
dukan sojojinsu. To, yanzu dai, ka daraja raina!"
15 Sai mala'ikan UBANGIJI ya ce wa Iliya, "Sauka, ka tafi tare da shi; kada ka ji tsoro."
Saboda haka Iliya ya tashi ya sauko, ya tafi tare da shi wajen sarki.
16 Iliya ya ce wa sarki, "Ga abin da UBANGIJI ya ce, don babu Allah a Isra'ila ne
wanda za ka tuntuɓa da ka aika a tuntuɓi Ba'al-Zebub, allahn Ekron? Domin ka yi
haka, ba za ka tashi daga gadon da kake kwance ba, ba shakka za ka mutu!" 17 Ya
kuwa mutu yadda UBANGIJI ya faɗa ta bakin Iliya.

Da yake Ahaziya ba shi da ɗa, sai Yoram[*] ya gāje shi, ya zama sarki a shekara ta
biyu ta mulkin Yehoram, ɗan Yehoshafat, sarkin Yahuda. 18 Game da dukan sauran
abubuwan da suka faru a zamani Ahaziya, da abin da ya yi, ba a rubuce suke a
littattafan tarihin sarakuna Isra'ila ba?

* **1:17** Da Ibraniyanci Yehoram, wani sunan Yoram.

# 2

*An ɗauki Iliya zuwa sama*

1 Da lokaci ya yi da UBANGIJI zai ɗauki Iliya zuwa sama cikin guguwa, Iliya da Elisha
kuwa suna kan hanyarsu daga Gilgal. 2 Sai Iliya ya ce wa Elisha, “Ka dakata a nan;
UBANGIJI ya aike ni Betel.”

Amma Elisha ya amsa ya ce, “Muddin UBANGIJI yana a raye, kai kuma kana a raye,
ba zan rabu da kai ba.” Saboda haka suka gangara zuwa Betel.

3 Sai ƙungiyar annabawa a Betel suka fito zuwa wajen Elisha suka ce masa, “Ka
san cewa UBANGIJI zai ɗauki maigidanka daga wurinka yau?”

Sai ya ce, “I, na sani, amma kada ku yi magana game da wannan.”

4 Sai Iliya ya ce masa, “Ka dakata a nan Elisha; UBANGIJI ya aike ni Yeriko.”

Sai ya ce masa, “Muddin UBANGIJI yana a raye, kai ma kana a raye, ba zan rabu da
kai ba.” Saboda haka sai suka tafi Yeriko.

5 Kungiyar annabawa a Yeriko suka haura zuwa wajen Elisha suka ce, “Ko ka san
UBANGIJI zai ɗauki maigidanka daga gare ka yau?”

Sai ya ce, “I, na sani, amma ku bar zancen nan tukuna.”

6 Sai Iliya ya ce masa, “Ka dakata a nan, UBANGIJI ya aike ni Urdun.”

Sai Elisha ya ce masa, “Muddin UBANGIJI yana a raye, kai kuma kana raye, ba zan
rabu da kai ba.” Saboda haka suka ci gaba da tafiya tare.

7 Mutum hamsin na ƙungiyar annabawa suka je suka tsaya da nisa, suna fuskantar
inda Iliya da Elisha suka tsaya a Urdun. 8 Sai Iliya ya tuɓe rigarsa, ya nannaɗe ya
bugi ruwan Urdun da shi. Sai ruwan ya dāre gida biyu, suka haye a busasshiyar
ƙasa.

9 Da suka haye, sai Iliya ya ce wa Elisha, “Faɗi mini, abin da kake so in yi maka
kafin a ɗauke ni daga gare ka!”

Elisha ya amsa ya ce, “Bari in gāji ninki biyu na ruhunka.”

10 Iliya ya ce, “Ka nemi abu mai wuya, amma in ka ga lokacin da aka ɗauke ni daga
gare ka, zai zama naka, in ba haka ba, ba za ka samu ba ke nan.”

11 Yayinda suke tafiya suna magana, sai kwatsam, keken yaƙin wuta da dawakan
wuta suka ratse tsakaninsu, sai Iliya ya tafi sama a cikin guguwa. 12 Da Elisha ya
ga haka sai ya yi ihu yana cewa, “Babana! Babana! Kekunan yaƙin da mahayan
dawakan Isra'ila!” Elisha kuwa bai sāke ganinsa ba. Sai ya kama tufafinsa ya
yayyage.

13 Sai ya ɗauki rigar da ta fāɗo daga Iliya ya koma ya tsaya a gaɓar Kogin Urdun.
14 Sa'an nan Elisha ya ɗauki rigar da ta fāɗo daga Iliya ya bugi ruwan da shi. Ya ce,
“Yanzu ina UBANGIJI Allah na Iliya?” Da ya bugi ruwan sai ruwan ya dāre gida biyu,
sai ya haye.

15 Kungiyar annabawa daga Yeriko, waɗanda suke kallo, suka ce, “Ruhun Iliya yana
a kan Elisha.” Sai suka je su tarye shi, suka rusuna har ƙasa a gabansa. 16 Suka ce,
“Duba, mu bayinka muna da masu ji da ƙarfi hamsin. Bari su je su nemi maigidanka.
Wataƙila, Ruhun UBANGIJI ya ɗauke shi ya ajiye bisa wani dutse, ko wani kwari.”

Elisha ya ce, “A'a, kada ku aike su.”

17 Amma suka matsa masa har ya ji ba ya iya hana su. Saboda haka ya ce, “Ku aike
su.” Sai suka aiki mutane hamsin, suka yi ta nema har kwana uku amma ba su same
Iliya ba. 18 Da suka dawo wurin Elisha, wanda yake a Yeriko, sai ya ce musu, “Ban
ce muku kada ku tafi ba?”

*Ruwan warkarwa*

19 Mutane garin suka ce wa Elisha, “Ranka yă daɗe, duba, garin yana da kyan gani,
amma ruwan ba shi da kyau, ƙasar kuma ba ta ba da amfani.”

20 Sai ya ce, “Ku kawo mini sabuwar ƙwarya, ku kuma sa gishiri a ciki.” Sai suka
kawo masa.
21 Sai ya tafi maɓulɓular ruwan yana watsa gishirin a ciki, yana cewa, “Ga abin
da UBANGIJI ya ce, ‘Na warkar da ruwan nan. Ba zai ƙara jawo mutuwa, ko yă hana
ƙasar ba da amfani ba.’ ” 22 Ruwan ya tsabtacce har yă zuwa yau, bisa ga faɗin Elisha.

*An yi wa Elisha dariya*

23 Daga nan sai Elisha ya tafi Betel. Yayinda yake tafiya a hanya, sai waɗansu
matasa suka fito daga cikin gari, suka yi masa dariya suna cewa, “Ka haura, ya kai
mai kai marar gashi! Ka haura, kai mai kai marar gashi!” 24 Sai ya juya ya dube su,
ya la’anta su da sunan UBANGIJI. Sai beyar guda biyu suka fito daga jeji suka hallaka
matasa arba’in da biyu daga cikinsu. 25 Sai ya ci gaba zuwa Dutsen Karmel, daga can
kuma ya koma Samariya.

# 3

*Mowab ta yi tawaye*

1 Yoram,* ɗan Ahab ya zama sarki Isra’ila, a Samariya, a shekara ta goma sha
takwas ta mulkin Yehoshafat, sarkin Yahuda, ya kuma yi mulki shekara goma sha
biyu. 2 Yoram ya aikata mugunta a gaban UBANGIJI, amma ba kamar yadda mahaifinsa
da mahaifiyarsa suka yi ba. Ya kawar da dutsen tsarkin Ba’al wanda mahaifinsa ya
yi. 3 Duk da haka ya manne wa zunuban Yerobowam ɗan Nebat, wanda ya sa Isra’ila
ta aikata, bai rabu da su ba.
4 Mesha, sarkin Mowab yana kiwon tumaki, ya kuma zama tilas yă biya haraji ga
sarkin Isra’ila. Saboda haka yakan ba da ’yan tumaki dubu ɗari, da kuma gashin
raguna dubu ɗari. 5 Amma bayan mutuwar Ahab, sai sarkin Mowab ya yi wa sarkin
Isra’ila tawaye. 6 To, a lokacin, Sarki Yoram ya tashi daga Samariya, ya tattara sojoji
daga dukan Isra’ila. 7 Ya kuma aika da wannan saƙo ga Yehoshafat sarkin Yahuda
cewa, “Sarkin Mowab ya yi mini tawaye. Za ka tafi tare da ni mu yaƙi Mowab?”

Sai sarkin Yahuda ya ce, “I, ina shirye mu tafi. Ai, sojojina sojojinka ne, dawakaina
kuma dawakanka ne.”
8 Ya ƙara da cewa, “Wace hanya za mu bi?”

Sai Yoram ya amsa ya ce, “Ta hanyar jejin Edom.”
9 Saboda haka sarkin Isra’ila ya fita tare da sarkin Yahuda, da kuma sarkin Edom.
Da suka yi kwana bakwai suna ta zagawa, sai sojoji da dabbobi suka rasa ruwan sha.
10 Sai sarkin Isra’ila ya ce, “Mene! UBANGIJI ya kira mu sarakunan nan uku don
kawai yă ba da mu ga Mowab ne?”
11 Amma Yehoshafat ya yi tambaya ya ce, “Babu wani annabin UBANGIJI a nan da
za mu nemi nufin UBANGIJI ta wurinsa?”

Wani hafsan sarkin Isra’ila ya amsa ya ce, “Ai, akwai Elisha ɗan Shafat, wanda dā
ya yi wa Iliya hidima.”
12 Yehoshafat ya ce, “Maganar UBANGIJI tana tare da shi.” Saboda haka sarkin
Isra’ila da Yehoshafat da kuma sarkin Edom suka tafi wurin Elisha.
13 Elisha ya ce wa sarkin Isra’ila, “Ina ruwana da kai? Tafi wurin annabawan
mahaifinka da annabawa mahaifiyarka.”

Sai sarkin Isra’ila ya ce, “A’a, ai UBANGIJI ne ya kira mu, mu sarakunan nan uku
don yă bashe mu ga Mowab.”
14 Sai Elisha ya ce, “Muddin UBANGIJI Maɗaukaki yana a raye, wanda nake bauta,
da ba don ina ganin girman Yehoshafat Sarkin Yahuda ba, da ko kallonka ba zan yi
ba. 15 Amma yanzu, a kawo mini makaɗin garaya.”

* **3:1** Ibraniyanci Yehoram, wani sunan Yoram; haka ma a aya 6.

Yayinda makaɗin garayan yake kiɗa, ikon UBANGIJI ya sauko a kan Elisha 16 ya kuma
ce, "Ga abin da UBANGIJI ya ce, zan cika kwarin nan da tafkunan ruwa. 17 Gama ga
abin da UBANGIJI ya ce, ko da yake babu iska, ko ruwan sama, duk da haka kwarin nan
zai cika da ruwa, har ku da dabbobinku da kuma sauran dabbobi ku sha. 18 Wannan
abu mai sauƙi ne a wurin UBANGIJI; zai kuma ba da Mowab a gare ku. 19 Za ku ci
kowane birni mai katanga, da kowane babban gari. Za ku sare kowane itace mai
kyau, ku kuma tattoshe maɓuɓɓugan ruwa. Za ku kuma yi amfani da duwatsu ku
lalatar da kowace gona mai kyau."

20 Kashegari, daidai lokacin hadaya, sai ga ruwa yana gangarowa daga gefen Edom!
Kasar kuwa ta cika da ruwa.

21 To, dukan Mowabawa suka ji cewa sarakuna suna tafe don su yaƙe su; saboda
haka aka kira kowane namiji, babba da yaro, wanda ya isa ɗaukan makami, aka jera
su a bakin iyaka. 22 Da suka tashi da sassafe, rana tana haska ruwa. Sai ruwan ya
yi ja kamar jini a idanun Mowabawan da suke a ƙetare. 23 Sai suka ce, "Jini ne! Ba
shakka sarakunan nan sun yaƙe juna, suka karkashe juna. Ya Mowabawa, mu tafi
mu kwashi ganima!"

24 Amma da Mowabawa suka isa sansanin Isra'ila, sai Isra'ilawa suka taso suka
auka musu har sai da suka gudu. Isra'ilawa kuwa suka kai musu hari, suka karkashe
Mowabawa. 25 Suka ragargaza garuruwa, kowane mutum kuwa ya jefa dutse a
kowane gona mai kyau har sai da aka rufe gonakin gaba ɗaya. Suka tattoshe duk
maɓulɓulan ruwa, suka kuma sare duk itace mai kyau. Kir Hareset ne kaɗai aka
bari tare da duwatsunsa yadda suke, amma mutanen da suke da majajjawa suka yi
wa birnin zobe, suka kai masa hari shi ma.

26 Da sarkin Mowab ya ga yaƙi ya rinjaye shi, sai ya ɗauki mutane masu takobi
ɗari bakwai, ya ratsa zuwa wajen sarkin Edom, amma ba su yi nasara ba. 27 Sa'an
nan ya ɗauki ɗansa na fari, wanda zai gāje shi, ya yi hadaya da shi a bisa katangan
birnin. Isra'ilawa suka firgita ƙwarai; sai suka janye suka koma ƙasarsu.

# 4

### *Man zaitun na gwauruwa*

1 Matar wani daga ƙungiyar annabawa ta yi wa Elisha kuka ta ce, "Mijina, bawanka,
ya mutu, ka kuma san yadda ya girmama UBANGIJI. Amma ga shi yanzu mai binsa
bashi ya zo yă kwashe 'ya'yana maza biyu su zama bayinsa."

2 Elisha ya amsa mata ya ce, "Me kike so in yi miki? Ki faɗa mini, me kike da shi
a gidanki?"

Sai ta ce, "Baiwarka ba ta da kome a can, sai ɗan tulun man zaitun."

3 Elisha ya ce, "Ki je wurin dukan maƙwabtanki, ki nemi tulunan da babu kome
a ciki. Kada ki nemo kaɗan kawai. 4 Sa'an nan ki shiga ciki, ki kulle ƙofar da ke da
'ya'yanki kuke ciki. Ku ɗuɗɗura man a dukan tulunan, sa'ad da kowanne ya cika,
sai ki ajiye a gefe."

5 Ta tashi ta shiga tare da 'ya'yanta maza, suka kulle ƙofa. 'Ya'yanta suka kawo
mata tuluna, ita kuma tana ɗurawa. 6 Da dukan tulunan suka cika, sai ta ce wa ɗanta,
"Kawo mini wani tulu."

Amma ya amsa ya ce, "Ai, ba saura." Sa'an nan man ya daina zuba.

7 Sai ta tafi ta faɗa wa mutumin Allah. Shi kuwa ya ce mata, "Tafi, ki sayar da man,
ki biya bashinki. Ki biya bukatanki da na 'ya'yanki da sauran da ya rage."

### *An maido da ɗan mutuniyar Shunem da rai*

8 Wata rana Elisha ya tafi Shunem. Akwai wata mai arziki a can wadda ta gayyace
shi cin abinci. Sai ya zama duk lokacin da yake wucewa, yakan tsaya a can don cin
abinci. 9 Ta ce wa mijinta, "Na san cewa wannan mutum da kullum yake zuwa nan

mai tsarki ne na Allah. 10 Bari mu yi ɗan ɗaki a rufin gida mu kuma sa masa gado
da tebur da kujera da kuma fitila. Saboda a duk lokacin da ya zo wurinmu, sai yă
sauka a can.”
11 Wata rana da Elisha ya zo, sai ya haura ɗakinsa ya kwanta. 12 Ya ce wa bawansa
Gehazi, “Kira mutuniyar Shunam nan.” Sai ya kira ta, ta zo ta tsaya a gabansa.
13 Elisha ya ce masa, “Ka ce mata, ‘Kin yi duk wannan ɗawainiya saboda mu. Yanzu,
me kike so a yi miki? Kina so mu yi magana a madadinki wa sarki ko babban hafsan
mayaƙa?’ ”
Sai ta ce, “A’a, ina da dukan abin da nake bukata a cikin jama’ata.”
14 Sai Elisha ya tambayi Gehazi ya ce, “Me za mu yi mata?”
Sai ya amsa ya ce, “Ba ta da ɗa, ga shi kuma mijinta ya tsufa.”
15 Sai Elisha ya ce, “Ka kira ta.” Sai ya kira ta, ta zo ta tsaya a bakin ƙofa. 16 Elisha
ya ce mata, “War haka baɗi, za ki riƙe ɗa na kanki.”
Sai ta ce masa, “A’a, ranka yă daɗe, mutumin Allah, kada ka ruɗi baiwarka!”
17 Amma matan ta yi ciki, a shekara ta biye kuwa a daidai lokacin, sai ta haifi ɗa
kamar yadda Elisha ya faɗa mata.
18 Yaron ya yi girma, wata rana sai ya tafi wurin mahaifinsa, wanda yake tare da
masu girbi. 19 Ba zato sai ya ce wa mahaifinsa, “Wayyo! Kaina yana mini ciwo! Kaina
yana mini ciwo!”
Sai mahaifinsa ya ce wa bawansa, “Kai shi wurin mahaifiyarsa.” 20 Bayan bawan
ya ɗaga shi ya kai wurin mahaifiyarsa, sai yaron ya zauna a cinyarta har tsakar rana,
sa’an nan ya mutu. 21 Sai ta haura ta shimfiɗa shi a gadon mutumin Allah, ta rufe
ƙofar, ta fita.
22 Ta kira mijinta ta ce, “Ina roƙonka ka aika mini da ɗaya daga cikin bayi da kuma
jaka, don in yi sauri in je wurin mutumin Allah in dawo.”
23 Sai ya ce, “Me zai kai ki wurinsa, ai, yau ba Sabon Wata ba ne ko ranar Asabbaci?”
Sai ta ce, “Ba kome.”
24 Sai ta sa wa jakar sirdi ta ce wa bawanta, “Yi ta kora mini jakar, kada ka sassauta,
sai na faɗa maka.” 25 Ta haka ta kama hanya ta tafi wurin mutumin Allah a Dutsen
Karmel.
Da ya hange ta daga nesa, sai mutumin Allah ya ce wa bawansa Gehazi, “Duba!
Ga mutuniyar Shunam nan can! 26 Ka yi gudu ka tarye ta ka tambaye ta, ‘Lafiyarki?
Mijinki yana nan lafiya? Yaronki yana nan lafiya?’ ”
Ta amsa ta ce, “Kome lafiya yake.”
27 Da ta isa wurin mutumin Allah a dutsen, sai ta kama ƙafafunsa. Sai Gehazi ya zo
don yă ture ta, amma mutumin Allah ya ce, “Ka bar ta! Tana cikin baƙin ciki ƙwarai,
amma UBANGIJI ya ɓoye mini, bai kuma faɗa mini me ya sa ba.”
28 Sai ta tambaya shi ta ce, “Na roƙe ka ɗa ne, ranka yă daɗe? Ba na ce maka,
‘Kada ka sa in fara bege ba’?”
29 Elisha ya ce wa Gehazi, “Ka yi ɗamara, ka ɗauki sandana ka ruga a guje. Idan
ka sadu da wani, kada ka gaishe shi, idan kuma wani ya gaishe ka, kada ka amsa. Ka
shimfiɗa sandana a fuskar yaron.”
30 Amma mahaifiyar yaron ta ce, “Muddin UBANGIJI yana raye, kai kuma kana a
raye, ba zan bar ka ba.” Saboda haka ya tashi ya bi ta.
31 Gehazi ya yi gaba, ya shimfiɗa sandan a fuskar yaron, amma babu motsi, babu
alamar rai. Saboda haka Gehazi ya koma ya taryi Elisha, ya faɗa masa, “Yaron bai
tashi ba.”
32 Da Elisha ya isa gidan, sai ga gawar yaron kwance a kan gadonsa. 33 Sai ya shiga,
ya rufe ƙofa, daga shi sai yaron, ya kuma yi addu’a ga UBANGIJI. 34 Sa’an nan ya hau
gadon yă kwanta a bisa yaron, ya miƙe a kansa, baki da baki, ido da ido, hannu da

hannu. Yayinda ya miƙe kansa a kan yaron, sai jikin yaron ya ɗau ɗumi. 35 Elisha ya
tashi, ya yi ta kai komo a cikin ɗakin. Sa'an nan ya sāke koma kan gadon yǎ miƙe a
kan yaron, sai yaron ya yi atishawa sau bakwai, ya kuma buɗe idanunsa.
36 Elisha ya kira Gehazi ya ce, "Kirawo mutuniyar Shunam." Ya kuwa kira ta. Sa'ad
da ta zo, sai Elisha ya ce mata, "Ɗauki ɗanki." 37 Sai ta shiga, ta fāɗi a ƙafafunsa ta
rusuna har ƙasa. Sa'an nan ta ɗauki ɗanta ta fita.

### *Mutuwa a tukunya*

38 Sai Elisha ya koma Gilgal, a can kuwa ana yunwa a yankin. Yayinda ƙungiyar
annabawa suke tattaunawa da shi, sai ya ce wa Gehazi bawansa, "Ka sa babban
tukunya a wuta, ka yi wa mutanen nan fate."
39 Ɗaya daga cikin mutanen ya shiga gona don neman ganyaye, ya kuwa sami
kabewar jeji. Ya tsinko 'ya'yanta cike da shafin rigarsa. Da ya dawo, sai ya yayyanka
su ya zuba a cikin tukunyar faten, ko da yake ba wanda ya san ko mene ne. 40 Sai
aka zuba wa mutanen faten, amma da suka fara ci, sai suka yi ihu suna cewa, "Ya
mutumin Allah, akwai dafi a cikin tukunyan nan!" Suka kuwa kāsa ci.
41 Elisha ya ce, "Samo mini ɗan gari." Aka kawo masa ya kuma sa a cikin tukunyan
ya ce, "Raba wa mutanen su ci." Ya kasance kuwa babu wani abin damuwa a
tukunyar.

### *Ciyar da mutum ɗari*

42 Sai ga wani mutum ya zo daga Ba'al-Shalisha, ya kawo wa Elisha dunƙulen
burodi guda ashirin na sha'ir da aka gasa daga nunan fari na hatsi, tare da kawunan
sababbin hatsi. Sai Elisha ya ce, "Ka ba mutanen su ci."
43 Sai bawansa ya ce, "Yaya zan raba wa mutane ɗari wannan?"
Amma Elisha ya amsa ya ce, "Ka raba wa mutane su ci, gama haka UBANGIJI ya ce,
'Za su ci har su bar saura.' " 44 Sa'an nan ya ajiye a gabansu, suka kuwa ci har suka
bar saura, bisa ga maganar UBANGIJI.

## 5

### *An warkar da Na'aman daga kuturta*

1 Na'aman babban hafsan hafsoshin rundunar sarkin Aram ne, kuma ƙasaitaccen
mutum ne mai martaba a idon maigidansa, domin ta wurinsa UBANGIJI ya ba Aram
nasara. Na'aman jarumi ne ƙwarai, amma yana da kuturta.
2 To, daga cikin hare haren da mutanen Aram suke kaiwa, sai suka kama wata
yarinya daga ƙasar Isra'ila, aka sa ta zama mai yi wa matar Na'aman aiki. 3 Sai ta ce
wa uwargijiyarta, "Da dai shugabana zai ga annabin da yake Samariya, da annabin
zai warkar da shi daga kuturtarsa."
4 Sai Na'aman ya je wurin maigidansa ya faɗa masa abin da yarinyan nan daga
Isra'ila ta faɗa. 5 Sarkin Aram ya ce, "Ko ta ƙaƙa, ka tafi, zan aika da wasiƙa ga sarkin
Isra'ila." Sai Na'aman ya tashi, ɗauke da talenti goma na azurfa, shekel dubu shida
na zinariya, da tufafi kashi goma. 6 Wasiƙar da ya kai wa sarkin Isra'ila ta ce, "Da
wannan wasiƙa ina aika Na'aman gare ka don ka warkar da kuturtarsa."
7 Da sarkin Isra'ila ya karanta wasiƙar, sai ya yayyage tufafinsa, ya ce, "Ni Allah ne?
Zan iya ɗauke rai ko in mai da shi? Me ya sa wannan mutum ya turo mini wannan
mutum in warkar da kuturtarsa? Dubi fa yadda yake nemana da faɗa!"
8 Da Elisha mutumin Allah ya ji cewa sarkin Isra'ila ya yayyage tufafinsa, sai ya
aika masa da wannan saƙo, "Don me za ka yayyage tufafinka? Ka sa mutumin yǎ
zo wurina, zai kuwa san cewa akwai annabi a Isra'ila." 9 Saboda haka Na'aman ya
tafi da dawakansa da keken yaƙinsa, ya tsaya a ƙofar gidan Elisha. 10 Sai Elisha ya

aika ʼyan saƙo su ce masa, “Je, ka nutse sau bakwai a Urdun, fatar jikinka za tă koma daidai, ka kuma tsarkaka.”

11 Amma Naʼaman ya tashi daga can da fushi yana cewa, “Na yi tsammani zai fito ne
wurina yă tsaya, yă yi kira bisa ga sunan UBANGIJI Allahnsa, yă kaɗa hannunsa inda
kuturtar take, yă warkar da ni. 12 Ashe, Amana da Farfa, kogunan da suke Damaskus,
ba su fi dukan ruwan da suke Israʼila ba? Me zai sa ba zan nutse cikinsu in tsarkaka
ba?” Sai ya juya ya yi tafiyarsa da fushi.

13 Sai bayin Naʼaman suka je kusa da shi suka ce, “Baba, da a ce annabin ya ce ka
yi wani abu mai wuya, da ba za ka yi ba? Balle fa cewa kawai ya yi, ‘Ka yi wanka ka
kuma tsarkaka’!” 14 Saboda haka Naʼaman ya je ya nutse sau bakwai a Urdun, yadda
mutumin Allah ya ce masa, sai fatarsa ta koma kamar ta ɗan yaro.

15 Sai Naʼaman da dukan masu hidimarsa suka koma wurin mutumin Allah.
Naʼaman ya tsaya a gaban mutumin Allah ya ce, “Yanzu na san cewa babu wani Allah a duk duniya sai a Israʼila. Ina roƙonka ka karɓi kyauta daga hannun bawanka.”

16 Annabin ya amsa ya ce, “Muddin UBANGIJI wanda nake bauta masa yana a raye, ba zan karɓi kome ba.” Ko da yake Naʼaman ya yi ta roƙonsa, amma ya ƙi.

17 Sai Naʼaman ya ce, “In ba za ka karɓa ba, ina roƙonka, bari a ba wa bawanka
ƙasa gwargwadon abin da jakuna biyu za su iya ɗauka, gama bawanka ba zai sāke
yin hadaya ta ƙonawa, ko wata hadaya ga wani allah ba, sai ga UBANGIJI. 18 Amma
ina fata UBANGIJI zai gafarta wa bawanka saboda abu guda. Bari yă gafarta mini sa'ad da na raka sarkina zuwa haikalin Rimmon domin yă yi sujada, bari UBANGIJI yă yi wa bawanka gafara saboda wannan.”

19 Sai Elisha ya ce, “Ka sauka lafiya.”

Bayan Naʼaman ya yi ɗan nisa, 20 sai Gehazi, bawan Elisha mutumin Allah, ya yi
tunani a ransa ya ce, “Maigidana ya yi wa Naʼaman mutumin Aram nan ƙaramci da bai karɓi duk abin da ya kawo ba. Muddin UBANGIJI yana a raye, zan bi shi a guje in karɓi wani abu daga gare shi.”

21 Saboda haka Gehazi ya bi Naʼaman a guje. Da Naʼaman ya hango shi yana zuwa a guje, sai ya sauka daga keken yaƙinsa ya tarye shi ya ce, “Lafiya?”

22 Gehazi ya amsa ya ce, “Lafiya ƙalau. Maigidana ne ya aiko ni cewa, ‘Samari biyu daga ƙungiyar annabawa sun ziyarce ni daga ƙasa mai duwatsu na yankin Efraim. Ina roƙonka ka ba su talenti na azurfa da tufafi kashi biyu.’ ”

23 Naʼaman ya ce, “Ba damuwa, karɓi talenti biyu.” Ya roƙi Gehazi yă karɓa, saʼan
nan ya ƙunsa masa talentin biyu na azurfa ya sa masa a kan jakankuna biyu, ya
haɗa da tufafi kashi biyu, ya ba bayinsa biyu suka ɗauka, ya ce su sha gaban Gehazi.
24 Da Gehazi ya isa wani tudu, sai ya karɓi kayan daga wurin bayin ya shiga da su a
ɓoye a cikin gida. Saʼan nan ya sallami mutanen suka tafi. 25 Saʼan nan ya shiga ya
tsaya a gaban maigidansa Elisha.

Sai Elisha ya tambaye shi ya ce, “Ina ka je, Gehazi?”

Sai Gehazi ya amsa ya ce, “Bawanka bai je koʼina ba.”

26 Amma Elisha ya ce masa, “Ashe, ba ina tare da kai a ruhu ba saʼad da mutumin ya sauko daga keken yaƙinsa ya tarye ka. Kana gani wannan lokaci ne da za a karɓi kuɗi, da riguna, da gonar inabi, da tumaki, da bijimai, da bayi maza da mata?
27 Kuturtar Naʼaman zai manne maka da zuriyarka har abada.” Sai Gehazi ya fita daga gaban Elisha a kuturce, fari fat kamar dusar ƙanƙara.

## 6

*Kan gatari ya yi yawo a kan ruwa*

1 Sai ƙungiyar annabawa suka ce wa Elisha, “Duba, wurin da muke taruwa ya
kāsa mana. 2 Bari mu je Urdun, inda kowannenmu zai saro itace; mu gina inda za
mu zauna.”
Sai ya ce musu, “Ku je.”
3 Sai ɗayansu ya ce, “Ba za ka zo tare da bayinka ba?”
Sai Elisha ya ce “Zan zo.” 4 Ya kuma tafi tare da su.
Suka tafi Urdun suka fara saran itatuwa. 5 Yayinda ɗayansu yake cikin saran itace,
sai kan gatarin ya fāɗi a ruwa, sai ya ce, “Kash, ranka yă daɗe, kayan aro ne fa!”
6 Sai mutumin Allah ya ce, “Daidai ina ya fāɗa?” Da ya nuna masa wurin, sai Elisha
ya yanka ɗan sanda ya jefa a wurin, ya sa kan gatarin ya taso sama. 7 Sai ya ce masa,
“Ka ɗauko.” Sai mutumin ya miƙa hannu ya ɗauka.

*Elisha ya yi wa makafi Arameyawa tarko*

8 To, fa, sarkin Aram yana yaƙi da Isra’ila. Bayan ya tattauna da hafsoshinsa, sai
ya ce, “Zan kafa sansanina a wurin kaza da kaza.”
9 Sai mutumin Allah ya aika wa sarkin Isra’ila cewa, “Ka yi hankali da wuce wuri
kaza, domin Arameyawa za su gangara can.” 10 Saboda haka sarkin Isra’ila ya lura
da inda mutumin Allah ya ambata. Sau da sau Elisha yakan yi wa sarki kashedi, don
haka ya riƙa taka yi tsantsan a wuraren nan.
11 Wannan ya husata sarkin Aram. Ya kira hafsoshinsa ya tambaye su ya ce, “Ku
faɗa mini, wane ne a cikinmu yake gefen sarkin Isra’ila?”
12 Sai ɗaya daga cikin hafsoshinsa ya ce, “Babu waninmu, ranka yă daɗe; Elisha,
annabin da yake a Isra’ila ne, yake faɗa wa sarkin Isra’ila dukan zancen da ka yi a
ɗakinka.”
13 Sai sarki ya ba da umarni ya ce, “Ku je ku tabbatar da inda yake don in aika
mutane a kamo shi.” Sai ya sami rahoto cewa, “Yana a Dotan.” 14 Sai ya aika da
dawakai da kekunan yaƙi da babban rukunin soja zuwa can. Suka bi dare, suka
kewaye birnin.
15 Sa’ad da bawan mutumin Allah ya farka ya kuma fita kashegari da sassafe, sai
ga mayaƙa tare da dawakai da kekunan yaƙi sun kewaye birni. Sai bawan ya ce,
“Ranka yă daɗe! Me za mu yi?”
16 Sai annabin ya ce, “Kada ka ji tsoro, waɗanda suke tare da mu sun fi waɗanda
suke tare da su.”
17 Sa’an nan Elisha ya yi addu’a ya ce, “Ya Ubangiji, ka buɗe idanunsa yă gani!”
Sai Ubangiji ya buɗe idanun bawan, ya duba, ya ga tuddai cike da dawakai da keken
yaƙin wuta kewaye da Elisha.
18 Yayinda abokan gāba suka gangaro wajensa, sai Elisha ya yi addu’a ga Ubangiji
ya ce, “Ka sa mutanen nan su zama makafi.” Sai Ubangiji ya buge su da makanta
kamar yadda Elisha ya roƙa.
19 Elisha ya ce musu, “Wannan ba ita ce hanyar ba, ba kuma gari ke nan ba, ku bi
ni, zan kuwa kai ku wurin mutumin da kuke nema!” Sai ya kai su Samariya.
20 Bayan suka shiga birnin, sai Elisha ya ce, “Ubangiji, ka buɗe idanun mutanen
nan don su gani.” Sa’an nan Ubangiji ya buɗe idanunsu suka ga kansu a tsakiyar
Samariya.
21 Da sarkin Isra’ila ya gan su, sai ya tambayi Elisha ya ce, “In kashe su ne,
mahaifina? In kashe su?”
22 Elisha ya ce, “Kada ka kashe su. Za ka kashe mutanen da ka kame da takobi
ko bakanka? Ka ba su abinci da ruwa su ci, su sha, sa’an nan su koma wurin
maigidansu.” 23 Saboda haka aka shirya musu babban liyafa, bayan sun ci, suka
kuma sha, sai ya tura su zuwa wurin maigidansu. Ta haka ’yan harin Aram suka
daina kai hari a yankin Isra’ila.

### *Yunwa a Samariya da aka kewaye da yaƙi*

24 Bayan wani lokaci, Ben-Hadad sarkin Aram ya tattara dukan rundunarsa, ya je ya
kewaye Samariya da yaƙi. 25 Aka yi babban yunwa a cikin birnin. Saboda daɗewar
wannan kewayewar da aka yi wa birnin, sai yunwa ta ɓarke a birnin, har ana sayar
da kan jaki a kan shekel tamanin, kashin kurciya kuma a kan shekel biyar.

26 Yayinda sarkin Isra'ila yake wucewa kusa da katanga, sai wata mace ta yi masa
kuka ta ce, "Ka taimake ni, ranka yă daɗe, sarki!"

27 Sai sarki ya amsa ya ce, "In Ubangiji bai taimake ki ba, me zan iya yi? Ina da
hatsi ko ruwan inabin da zan ba ki ne?" 28 Sa'an nan ya tambaye ta ya ce, "Me ya
faru?"

Sai ta amsa ta ce, "Wannan mace ta ce mini, 'Kawo ɗanki mu ci yau, gobe kuwa
mu ci ɗana.' 29 Saboda haka muka dafa ɗana muka ci. Kashegari na ce mata, 'Kawo
ɗanki mu ci,' amma ta ɓoye shi."

30 Da sarki ya ji maganar macen sai ya yage rigunansa. Sa'ad da sarki yake wucewa
a kan katangar birnin, sai mutane suka gan yana saye da rigar makoki a ciki. 31 Ya
ce, "Bari Allah yă yi mini hukunci mai tsanani har ma fiye da haka, idan ban cire
kan Elisha ɗan Shafat yau ba!"

32 To, Elisha yana zaune a cikin gidansa, dattawa kuwa suna zaune tare da shi.
Sai sarki ya aiki ɗan aika yă ci gaba, amma kafin ɗan aikan yă isa, Elisha ya ce wa
dattawan, "Kun gani ko? Wannan mai kisa ya aiko a cire mini kai! To, idan ɗan aikan
ya iso, sai ku rufe ƙofar da ƙarfi, ku bar shi a waje. Ba da jimawa ba, maigidansa zai
bi bayansa?" 33 Yana magana da su ke nan, sai ga ɗan aikan ya gangaro wajensa.

Sarki kuma ya ce, "Wannan bala'in daga wurin Ubangiji ya fito. Don me zan sa
zuciya ga Ubangiji kuma?"

# 7

1 Sai Elisha ya ce, "Ku ji maganar Ubangiji. Ga abin da Ubangiji ya ce, gobe war
haka, za a sayar da mudun gari mai laushi a farashin shekel guda, mudu biyu na
sha'ir kuma a shekel ɗaya a ƙofar birnin Samariya."

2 Sai wani hafsa mataimakin sarki ya ce wa mutumin Allah, "Kai, ko da Ubangiji
zai buɗe tagogin sama, wannan abu ba zai yiwu ba!"

Sai Elisha ya ce, "Za ka gani da idanunka, zai faru, amma ba za ka ci ba!"

### *An daina kwanton ɓauna*

3 To, akwai waɗansu kutare huɗu a ƙofar gari. Suka ce wa junansu, "Don me za
mu zauna a nan sai mun mutu? 4 In muka ce, 'Za mu shiga cikin birni' yunwa tana
can, za mu kuwa mutu. Idan kuwa muka zauna a nan, za mu mutu. Saboda haka,
bari mu ƙetare zuwa sansanin Arameyawa mu miƙa kai. Idan suka bar mu da rai,
to; idan kuwa suka kashe mu, shi ke nan."

5 Da yamma sai suka tashi suka tafi sansanin Arameyawa. Yayinda suka shiga
tsakiyar sansanin Arameyawa kuwa, sai suka tarar ba kowa a can, 6 gama Ubangiji
ya sa rundunar Arameyawa suka ji motsin kekunan yaƙi, da motsin dawakai, da na
babban rundunar sojoji, saboda haka suka ce wa juna; "Duba, sarkin Isra'ila ya ɗauka
hayar sarakuna Hittiyawa da sarakunan Masarawa don su yaƙe mu!" 7 Saboda haka
suka tashi, suka gudu da yamma, suka bar tentunansu, da dawakansu, da jakunansu.
Suka bar sansanin yadda yake, suka gudu don su ceci rayukansu.

8 Da kutaren nan suka kai bakin sansanin, sai suka shiga wani tenti, suka ci, suka
sha, suka kwashi azurfa, da zinariya, da riguna, suka tafi, suka ɓoye su. Sa'an nan
suka koma, suka shiga wani tenti, sai suka kwashi kaya daga ciki, suka kuma ɓoye
su.

9 Sa'an nan suka ce wa juna, “Ba mu yi abin kirki ba. Wannan rana ce ta albishiri
amma muka yi shiru; in kuwa mun bari har gari ya waye, to, fa, wata masifa za tă
fāɗo mana. Bari mu tafi nan take mu faɗa a fadan sarki.”
10 Saboda haka suka je suka kira masu tsaron ƙofar birni, suka ce musu, “Mun je
sansanin Arameyawa, ga shi kuwa ba mu iske kowa a can ba, babu ko motsin wani,
sai dai dawakai da jakuna a daure, tentunan kuwa suna nan yadda suke.” 11 Sai
matsaran ƙofar suka sanar da labarin a cikin fada.
12 Sai sarki ya tashi da daren nan ya ce wa hafsoshinsa, “Na san abin da
Arameyawan suke shiri! Sun san game da yunwar da muke ciki a nan, domin haka
sun bar sansaninsu suka shiga jeji suka ɓuya, suna nufin sa'ad da muka fita daga
birni, sai su kama mu da rai, sa'an nan su shiga birnin.”
13 Ɗaya daga cikin fadawan sarki ya ce, “A sa waɗansu mutane su ɗauki dawakai
biyar da suka ragu cikin birni, idan ba su tsira ba, za su zama kamar sauran
Isra'ilawan da suka riga suka mutu ne. Bari mu aika, mu gani.”
14 Saboda haka suka zaɓi kekunan yaƙi biyu tare da dawakansu, sarki kuwa ya
aike su su bi bayan sojojin Arameyawa. Ya umarci masu tuƙinsu ya ce, “Ku je ku
bincika abin da ya faru.” 15 Suka bi sawunsu har Urdun, suka ga tufafi da makamai
barjat ko'ina a hanya waɗanda Arameyawa suka zubar yayinda suke gudu. Sai 'yan
aika suka dawo suka ba wa sarki labari. 16 Sa'an nan jama'a suka fita suka kwashi
ganima a sansanin Arameyawa. Aka kuwa sayar da gari mai laushi a farashin shekel
guda, mudu biyu na sha'ir kuma a shekel guda, yadda UBANGIJI ya faɗi.
17 Sai ya kasance cewa Sarki ya sa dogari wanda ya raka shi wajen Elisha ya tsare
ƙofar birnin. Sai mutane suka tattake shi a ƙofar har ya mutu, kamar yadda annabi
Elisha ya faɗa sa'ad da sarki ya tafi wurinsa. 18 Haka kuwa ya kasance kamar yadda
mutumin Allah ya ce wa sarki, “Gobe war haka, za a sayar da mudun gari shekel
guda, mudun sha'ir biyu ma a shekel guda, a ƙofar Samariya.”
19 Hafsan ya riga ya ce wa mutumin Allah, “Kai, ko da UBANGIJI zai buɗe tagogin
sama, wannan abu ba zai yiwu ba!” Mutumin Allah kuwa ya faɗa masa, “Za ka gani
da idanunka sai dai ba za ka ci ba!” 20 Haka kuwa ya kasance, gama mutane sun
tattake shi a hanyar shiga, har ya mutu.

# 8

*An maido da ƙasar mutanen Shunem*

1 To, Elisha ya riga ya ce wa matan da ya tā da ɗanta daga matattu, “Ki kwashe
iyalinki ku tafi duk inda za ku tafi na ɗan lokaci, domin UBANGIJI ya sa a yi yunwa
na shekara bakwai a ƙasar.” 2 Sai macen ta yi kamar yadda mutumin Allah ya faɗa.
Ita da iyalinta suka tafi ƙasar Filistiyawa suka zauna shekara bakwai.
3 A ƙarshen shekara bakwai ɗin sai ta dawo daga ƙasar Filistiyawa, ta kuma tafi
wajen sarki ta roƙa a mayar mata da gidanta da filinta. 4 Sarki kuwa yana magana
da Gehazi bawan mutumin Allah, ya ce masa, “Ba ni labarin dukan abubuwan
banmamakin da Elisha ya yi.” 5 A sa'ad da Gehazi yana cikin ba shi labarin yadda
Elisha ya tā da matacce ke nan, sai ga macen da aka tā da ɗanta daga matattu ta
shigo don tă roƙi sarki yă mayar mata da gidanta da filinta.

Gehazi ya ce, “Ranka yă daɗe, ai, ga macen, ga kuma ɗan da Elisha ya tā da daga
matattu.” 6 Sarki ya tambayi macen game da al'amarin, ita kuwa ta faɗa masa.

Sa'an nan ya sa wani hafsa yă dubi damuwarta ya kuma ce masa, “Ka mayar mata
kome da yake nata, haɗe da dukan kuɗin da aka samo daga filin, daga ranar da ta
bar ƙasar har yă zuwa yanzu.”

*Hazayel ya kashe Ben-Hadad*

7 Sai Elisha ya tafi Damaskus, Ben-Hadad mutumin Aram kuwa yana ciwo. Sa'ad
da aka faɗa wa sarki, "Mutumin Allah ya hauro tun daga can zuwa nan," 8 sai ya
ce wa Hazayel, "Dauki wannan tare da kai ka tafi ka taryi mutumin Allah. Ka nemi
nufin UBANGIJI ta wurinsa; ka tambaye shi, 'Zan warke daga ciwon nan?' "
9 Sai Hazayel ya tafi taryen Elisha, ya ɗauka kyauta na kowane irin kaya masu kyau
na Damaskus tare da shi a raƙuma arba'in. Ya shiga ya tsaya a gaban Elisha ya ce,
"Danka Ben-Hadad na Aram ya aike ni in tambaye ka, 'Zan warke daga ciwon nan?' "
10 Elisha ya amsa ya ce, "Je ka ce masa, 'Ba shakka za ka warke'; amma* UBANGIJI
ya nuna mini cewa ba shakka zai mutu." 11 Sai ya zuba wa Hazayel ido har sai da
Hazayel ya ji kunya. Sa'an nan mutumin Allah ya fara kuka.
12 Hazayel ya ce masa, "Me ya sa ranka yă daɗe yake kuka?"
Elisha ya amsa, "Domin na san illar da za ka yi wa Isra'ilawa. Za ka ƙona biranensu
masu katanga, ka karkashe majiya ƙarfinsu da takobi, ka fyaffyaɗe ƙananan yaransu
da ƙasa, ka tsattsage matansu masu ciki."
13 Hazayel ya ce, "Yaya bawanka, wanda yake kare kawai, zai iya aikata wannan
irin abu?"
Elisha ya ce, "UBANGIJI ya nuna mini cewa za ka zama sarkin Aram."
14 Sai Hazayel ya rabu da Elisha ya koma wurin maigidansa. Da Ben-Hadad ya
yi tambaya, "Me Elisha ya ce maka?" Sai Hazayel ya amsa, "Ya faɗa mini cewa
tabbatacce za ka warke." 15 Amma kashegari sai ya ɗauki tsumma mai kauri, ya jiƙa
shi, ya rufe fuskar sarki da shi, har sai da sarki ya mutu. Sai Hazayel ya gāje shi a
matsayin sarki.

*Yehoram sarkin Yahuda*
*(2 Tarihi 21.2-20)*

16 A shekara ta biyar ta mulkin Yoram ɗan Ahab, sarkin Isra'ila, sa'ad da Yehoshafat
yake sarautar Yahuda, Yoram ɗan Yehoshafat, ya fara mulkinsa a matsayin sarkin
Yahuda. 17 Yana da shekara talatin da biyu sa'ad da ya zama sarki, ya kuma yi mulki
na tsawon shekara takwas a Urushalima. 18 Ya bi gurbin sarakunan Isra'ila, yadda
gidan Ahab ta yi, gama ya auri 'yar Ahab. Ya yi mugunta a gaban UBANGIJI. 19 Duk
da haka, saboda bawansa Dawuda, UBANGIJI bai ragargaza Yahuda ba. Ya riga ya yi
alkawari zai bar wa Dawuda magāji har abada.
20 A kwanakin Yoram, Edom ta yi wa Yahuda tawaye, ta naɗa wa kanta sarki.
21 Saboda haka Yehoram ya tafi Zayir da dukan kekunan yaƙinsa. Sojojin Edom suka
kewaye shi a can, amma da dare sai Yoram ya ɓarke ya gudu, sojojinsa kuma suka
watse zuwa gidajensu. 22 Har yă zuwa yau, Edom tana yi wa Yahuda tawaye. A lokaci
ɗaya ne Libna ma ta yi tawaye.
23 Game da waɗansu abubuwan da suka faru a zamanin Yoram, ba suna a rubuce a
cikin littafin tarihin sarakunan Yahuda ba? 24 Yoram ya huta tare da kakanninsa, aka
kuma binne shi a birnin Dawuda. Sai Ahaziya ɗansa ya gāje shi a matsayin sarki.

*(2 Tarihi 22.1-6)*

25 A shekara ta goma sha biyu ta Yoram ɗan Ahab, sarkin Isra'ila, Ahaziya ɗan
Yehoram, sarkin Yahuda ya fara mulki. 26 Ahaziya yana da shekara ashirin da
biyu sa'ad da ya zama sarki, ya kuma yi mulki a Urushalima shekara ɗaya. Sunan
mahaifiyarsa Ataliya, jikanyar Omri, sarkin Isra'ila. 27 Ya bi gurbin gidan Ahab, ya yi
mugunta a gaban UBANGIJI yadda gida Ahab ta yi, gama yana da dangantaka ta aure
da gidan Ahab.
28 Ahaziya ya tafi tare da Yoram ɗan Ahab don su yaƙi Hazayel sarkin Aram a
Ramot Gileyad. Arameyawa suka yi wa Yoram rauni; 29 saboda haka Sarki Yoram ya

* **8:10** Za a iya karanta Ibraniyanci haka Tafi ka kuma ce, "Tabbatacce ba za ka warke ba," gama

koma zuwa Yezireyel don yǎ yi jinyar raunin da Arameyawa suka ji masa a Rama a yaƙinsa da Hazayel sarkin Aram.

Sai Ahaziya ɗan Yehoram, sarkin Yahuda ya gangara zuwa Yezireyel yǎ dubi Yoram ɗan Ahab domin an yi masa rauni.

# 9

### *An naɗa Yehu sarkin Isra'ila*

1 Sai Elisha ya kira wani daga cikin ƙungiyar annabawa, ya ce masa, "Ka sha
ɗamara, ka ɗauki wannan kwalabar mai ka je Ramot Gileyad. 2 Da ka isa can, ka
nemi Yehu ɗan Yehoshafat, ɗan Nimshi. Ka je wurinsa, ka ja shi gefe daga abokansa,
ka shiga da shi ɗaki na ciki. 3 Sa'an nan ka ɗauki kwalabar man ka zuba a kansa, ka
ce, 'Ga abin da UBANGIJI ya faɗa, na naɗa ka sarkin Isra'ila.' Sa'an nan ka buɗe ƙofa
ka ruga a guje; kada ka ɓata lokaci!"
4 Sai saurayin nan, annabi, ya tafi Ramot Gileyad. 5 Da ya isa can, sai ya tarar da
hafsoshin soji zaune a wuri guda. Sai ya ce, "Ina da saƙo dominka komanda."

Sai Yehu ya ce, "Wanne a cikinmu?"

Sai ce, "Dominka, komanda."

6 Sai Yehu ya tashi ya shiga cikin gida. Sa'an nan annabin ya zuba wa Yehu mai
a kā, ya ce, "Ga abin da UBANGIJI, Allah na Isra'ila ya ce, 'Na naɗa ka sarki a bisa
jama'ar UBANGIJI, wato, Isra'ila. 7 Za aka hallaka gidan Ahab maigidanka, zan kuma
ɗauki fansar jinin bayina annabawa da kuma jinin dukan bayin UBANGIJI da Yezebel
ta zub da. 8 Dukan gidan Ahab zai hallaka. Zan kashe dukan 'ya'yan Ahab maza a
Isra'ila, bayi ko 'yantattu. 9 Zan mai da gidan Ahab kamar gidan Yerobowam ɗan
Nebat da kuma kamar gidan Ba'asha ɗan Ahiya. 10 Game da Yezebel kuwa, karnuka
za su cinye ta a fili a Yezireyel, ba kuwa wanda zai binne ta.' " Sa'an nan ya buɗe
ƙofa ya ruga a guje.
11 Da Yehu ya koma wurin sauran hafsoshin sai ɗaya daga cikinsu ya tambaye shi,
"Lafiya? Me ya kawo wannan mahaukaci a wurinka?"

Sai Yehu ya ce, "Ka san mahaukacin nan da irin maganganunsa."

12 Suka ce masa, "Ba gaskiya ba ne, ka dai faɗa mana."

Yehu ya ce, "Ga abin da ya ce mini, 'Ga abin da UBANGIJI ya ce, na naɗa ka sarki a
bisa Isra'ila.' "
13 Sai suka yi sauri suka ɗauki rigunansu suka shimfiɗa a ƙasa, suka busa kakaki,
suka yi ihu, suka ce, "Yehu ne sarki."

### *Yehu ya kashe Yoram da Ahaziya*

14 Saboda haka, Yehu ɗan Yehoshafat, ɗan Nimshi, ya ƙulla wa Yoram
maƙarƙashiya (To, Yoram da dukan Isra'ila suna kāre Ramot Gileyad daga Hazayel
sarkin Aram, 15 amma Sarki Yoram ya koma Yezireyel don yǎ farfaɗo daga raunukan
da Arameyawa suka ji masa a wata gabzawar da ya yi da Hazayel sarkin Aram.)
Yehu ya ce, "In haka kuke ji, kada ku bar wani yǎ sulluɓe daga birnin yǎ kai labarin
Yezireyel." 16 Sai ya tashi ya ɗauki keken yaƙinsa ya tafi Yezireyel gama Yoram yana
hutawa a can. Ga kuma Ahaziya sarkin Yahuda ya je don yǎ gan shi.
17 Mai tsaro kuwa yana tsaye a kan hasumiya a Yezireyel, sai ya hangi rundunar
Yehu sa'ad da yake zuwa. Ya ce, "Na ga wata runduna."

Sai Yoram ya umarta, "Nemi mahayin doki a aike shi yǎ tarye su, yǎ kuma tambaye su, 'Lafiya?' "
18 Sai mahayin dokin ya hau, ya ruga, ya taryi Yehu, ya ce, "Ga abin da sarki ya ce,
'Lafiya?' "

Sai Yehu ya ce masa, "Ina ruwanka da zancen lafiya? Ka shiga layi."

Sai mai tsaron ya ce wa sarki, "Dan saƙon ya kai wurinsu, amma ba ya dawowa."

19 Saboda haka sarki ya sāke aika mahayin doki na biyu. Sa'ad da ya isa wurinsu
sai ya ce, "Ga abin da sarki ya ce, 'Lafiya?' "
Yehu ya ce, "Ina ruwanka da zancen lafiya? Ka shiga layi."
20 Mai tsaro ya sāke cewa, "Ya kai wurinsu, amma shi ma ba ya dawowa. Ina ganin
sukuwar kamar irin ta Yehu, jikan Nimshi, gama yakan yi sukuwa kamar mahaukaci."
21 Yoram ya umarta, "Haɗa mini keken yaƙi!" Da aka haɗa, sai Yoram sarkin
Isra'ila, da Ahaziya sarkin Yahuda, suka hau suka tafi, kowa a keken yaƙinsa, don su
taryi Yehu. Suka sadu da shi a filin da yake na Nabot mutumin Yezireyel. 22 Sa'ad da
Yoram ya ga Yehu sai ya tambaye shi, "Lafiya kuwa ka zo, Yehu?"
Yehu ya ce, "Ina kuwa lafiya, da yake dukan bautar gumaka da bokancin
mahaifiyarka Yezebel sun bazu ko'ina?"
23 Yoram ya juya, ya gudu, yana ce wa Ahaziya, "Cin amana, Ahaziya!"
24 Sai Yehu ya ja bakansa ya harbi Yoram a tsakanin kafaɗunsa. Kibiyar ta same shi
a zuciyarsa sai ya fāɗi a cikin keken yaƙinsa. 25 Yehu ya ce wa Bidkar, hafsan keken
yaƙinsa, "Ka ɗauke shi ka jefar a filin da yake na Nabot mutumin Yezireyel. Ka tuna
yadda ni da kai muke a kekunan yaƙi a bayan Ahab mahaifinsa sa'ad da UBANGIJI
ya yi wannan annabci game da shi, 26 'Jiya na ga jinin Nabot da jinin 'ya'yansa, in
ji UBANGIJI, kuma ba shakka zan ɗauki fansa a wannan fili, in ji UBANGIJI.' Saboda
haka, ka ɗauke shi ka jefar da shi a bisa wannan fegi, bisa ga faɗin UBANGIJI.* Saboda
haka, ka ɗauke shi ka jefar a filin, in ji UBANGIJI."
27 Sa'ad da Ahaziya sarkin Yahuda ya ga abin da ya faru, sai ya haura hanyar Bet
Haggan a guje.† Yehu ya bi shi yana ihu, "A kashe shi, shi ma!" Suka ji masa rauni
a keken yaƙinsa a hanya zuwa Gur, kusa da Ibileyam amma ya tsere zuwa Megiddo
ya mutu a can. 28 Barorinsa suka ɗauke shi cikin keken yaƙi zuwa Urushalima suka
binne shi a kabarinsa tare da kakanninsa a birnin Dawuda. 29 (A shekara ta goma
sha ɗaya ta Yoram ɗan Ahab, Ahaziya ya zama sarkin Yahuda.)

### *Mutuwar Yezebel*

30 Sa'an nan Yehu ya je Yezireyel. Sa'ad da Yezebel ta sami labari, sai ta sha kwalliya
ta gyara gashin kanta, ta zauna tana kallo daga taga. 31 Yayinda Yehu ya shiga ƙofa,
sai ta ce, "Lafiya, kai Zimri, mai kashe maigidansa?"‡
32 Sai ya ɗaga ido ya dubi tagan ya ce, "Wa yake gefena? Wane ne?" Sai bābānni
biyu ko uku suka leƙo suka dube shi. 33 Yehu ya ce musu, "Ku jefa ta ƙasa!" Sai suka
jefar da ita, jininta ya fantsama a jikin bango da kuma a jikin dawakai yayinda suke
tattaka ta.
34 Yehu ya shiga ya ci, ya kuma sha. Ya ce, "Ku san yadda za ku yi da la'ananniyan
nan, ku binne ta, gama 'yar sarki ce." 35 Amma sa'ad da suka je don su binne ta, ba
su sami kome ba sai ƙoƙon kanta, ƙafafunta da kuma hannuwanta. 36 Suka komo
suka faɗa wa Yehu, wanda ya ce, "Wannan ita ce maganar da UBANGIJI ya faɗa ta
bakin bawansa Iliya mutumin Tishbe. A fili, a Yezireyel, karnuka za su cinye naman
Yezebel.§ 37 Gawar Yezebel zai zama kamar juji a ƙasa, a fili, a Yezireyel, har ba
wanda zai iya cewa, 'Wannan Yezebel ce.' "

# 10

### *An kashe iyalin Ahab*

1 To, akwai 'ya'ya maza saba'in na gidan Ahab a Samariya. Saboda haka Yehu ya
rubuta wasiƙu, ya aika su Samariya, zuwa ga shugabannin Yezireyel, da kuma ga
masu lura da 'ya'yan Ahab. Ya ce, 2 "Da zarar wasiƙan nan ta sadu da ku, da yake

* **9:26** Dubi 1Sar 21.19. † **9:27** Ko kuwa ya gudu ta hanyar lambun gida ‡ **9:31** Ko kuwa "Zimri yana da salama kuwa, shi da ya kashe maigidansa?" § **9:36** Dubi 1Sar 21.23.

ʼyaʼyan maigidanku suna tare da ku, kuna kuma da kekunan yaƙi da dawakai, da
birni mai katanga da makamai, 3 sai ku zaɓi mafi cancanta a cikin ʼyaʼyan maigidanku
ku sa shi a kan kursiyin mahaifinsa. Saʼan nan ku yi yaƙi don gidan maigidanku."

4 Amma suka razana suka ce, "Idan sarakuna biyu ba su iya yin tsayayya da shi ba,
wane mu?"

5 Saboda haka sarkin fada, da gwamnan birnin, da dattawa, da kuma masu lura da
ʼyaʼyan suka aika da saƙo ga Yehu, cewa, "Mu bayinka ne, za mu kuma yi duk abin
da ka ce. Ba za mu naɗa kowa sarki ba; sai ka yi abin da ka ga ya fi kyau."

6 Sai Yehu ya sāke rubuta musu wasiƙa ta biyu, ya ce, "In a gefena kuke, to, sai ku
yi biyayya da ni, ku fille kawunan ʼyaʼyan maigidanku, ku kawo mini a Yezireyel war
haka gobe."

To, ʼyaʼyan sarki, su sabaʼin, suna tare da manyan birni waɗanda suke lura da
su. 7 Saʼad da wasiƙar ta iso, sai mutanen nan suka ɗauki dukan ʼyaʼyan sarkin nan
sabaʼin, suka kashe su, suka sa kawunansu cikin kwanduna, suka aika wa Yehu a
Yezireyel. 8 Da ɗan saƙon ya iso, sai aka ce wa Yehu, "Sun kawo kawunan ʼyaʼyan
sarki."

Sai Yehu ya ce, "Ku ajiye su kashi biyu a ƙofar gari har safiya."

9 Da gari ya waye, sai Yehu ya fita ya tsaya a gaban dukan jamaʼa ya ce, "Ba ku
da laifi. Ni ne na ƙulla wa maigidana maƙarƙashiya, na kuma kashe shi, amma wa
ya karkashe dukan waɗannan? 10 Ku sani fa, ba kalmar da Ubangiji ya faɗa game
da gidan Ahab da ba za tă cika ba. Ubangiji ya yi abin da ya alkawarta ta bakin
bawansa Iliya." 11 Saboda haka Yehu ya kashe duk waɗanda suka rage na iyalin
Ahab a Yezireyel, tare da dukan fadawansa da aminansa da firistocinsa, ba a bar
masa kowa ba.

12 Saʼan nan Yehu ya nufi Samariya. Da ya kai Bet-Eked na Makiyaya, 13 sai ya gamu
da waɗansu daga dangin Ahaziya sarkin Yahuda, sai ya tambaye su, ya ce, "Ku, su
wane ne?"

Suka ce, "Mu dangin Ahaziya ne, mun kuma zo ne mu gai da iyalan sarki da kuma
mahaifiyar sarauniya."

14 Sai ya umarta ya ce, "A kama su da rai!" Aka kuwa kama su aka yayyanka kusa
da rijiyar Bet-Eked, su arbaʼin da biyu. Ba a bar wani da rai ba.

15 Bayan ya bar wurin, sai ya gamu da Yehonadab ɗan Rekab wanda yake kan
hanyarsa don yă sadu da shi. Sai Yehu ya gaishe shi, ya ce, "Ka amince da ni yadda
na amince da kai?"

Yehonadab ya ce, "I."

Yehu ya ce, "To, in haka ne ka ba ni hannunka." Sai ya miƙa masa, Yehu kuwa ya ja
shi cikin keken yaƙin. 16 Yehu ya ce, "Zo tare da ni ka ga himmata saboda Ubangiji."
Saʼan nan ya sa suka tafi tare cikin keken yaƙinsa.

17 Da Yehu ya isa Samariya, sai ya karkashe dukan sauran iyalin Ahab, ya hallaka
su, bisa ga maganar da Ubangiji ya faɗa ta bakin Iliya.

### *An kashe masu hidimar Baʼal*

18 Saʼan nan Yehu ya tattara dukan jamaʼa ya ce musu, "Ahab ya bauta wa Baʼal
kaɗan ne kawai; amma Yehu zai bauta masa sosai. 19 Yanzu sai ku kira dukan
annabawan Baʼal, dukan masu yin masa hidima da kuma dukan firistocinsa. Ku
tabbata ba a manta da wani ba, gama zan yi wa Baʼal babbar hadaya. Duk wanda
bai zo ba, a bakin ransa." Amma Yehu yana wayo ne domin yă hallaka masu yi wa
Baʼal sujada.

20 Yehu ya ce, "Ku kira jamaʼa don a girmama Baʼal." Saboda haka suka yi shela.
21 Saʼan nan ya aika saƙo koʼina a Israʼila, dukan masu yi wa Baʼal hidima kuwa suka
tattaru, ba mutumin da bai zo ba. Suka yi cincirindo a haikalin Baʼal har sai da ya

cika makil. 22 Sai Yehu ya ce wa mai ajiyar tufafi, “Ka kawo riguna domin dukan
masu yi wa Ba’al hidima.” Sai ya fito musu da riguna.
23 Sa’an nan Yehu da Yehonadab ɗan Rekab, suka shiga haikalin Ba’al. Yehu ya
ce wa masu yi wa Ba’al sujada, “Ku dudduba ku tabbatar cewa babu wani bawan
Ubangiji a nan tare da ku, sai masu hidimar Ba’al kawai.” 24 Saboda haka suka shiga
don su miƙa hadayu da kuma hadaya ta ƙonawa. To, Yehu ya riga ya ba wa mutane
takwas wannan kashedi a waje cewa, “In waninku ya bar ɗaya daga cikin mutanen
nan da nake danƙa a hannunku ya tsere, to, a bakin ransa.”
25 Nan da nan sa’ad da Yehu ya gama yin hadayar, sai ya umarci masu gadin da
hafsoshi, “Ku shiga ku karkashe su; kada ku bar wani yǎ tsere.” Saboda haka suka
karkashe su da takobi. Masu gadin da hafsoshin suka wuwwurga gawawwakinsu
waje, suka kuma shiga ciki cikin haikalin Ba’al ɗin, 26 suka fitar da dutsen tsafi daga
haikalin Ba’al, suka kuma ƙone shi. 27 Suka farfasa dutsen tsafin Ba’al, suka kuma
rushe haikalin, mutane suka mai da wurin salga har yǎ zuwa yau.
28 Ta haka Yehu ya hallaka butar Ba’al a Isra’ila. 29 Duk da haka, bai rabu da
zunuban Yerobowam ɗan Nebat, wanda ya sa Isra’ila ta aikata ba, wato, yin sujada
ga siffofin maruƙa na zinariya a Betel da kuma Dan.
30 Ubangiji ya ce wa Yehu, “Tun da yake ka aikata abin da yake mai kyau a idanuna,
ka kuma yi wa gidan Ahab dukan abin da yake a zuciyata, ina yin maka alkawari
cewa zuriyarka za su yi mulkin Isra’ila har tsara ta huɗu.” 31 Duk da haka, Yehu bai
mai da hankali ya kiyaye dokokin Ubangiji, Allah na Isra’ila da dukan zuciyarsa ba.
Bai rabu da zunubin Yerobowam, wanda ya sa Isra’ila ta aikata ba.
32 A kwanakin sai Ubangiji ya fara rage girman Isra’ila, Hazayel ya yi nasara a bisa
Isra’ila a ko’ina a yankinsu 33 gabas da Urdun, cikin dukan ƙasar Gileyad (yankin Gad,
da na Ruben, da na Manasse), daga Arower wajen Kwarin Arnon ya ratsa Gileyad
zuwa Bashan.
34 Game da sauran ayyukan mulkin Yehu, da dukan abin da ya yi, a rubuce suke a
cikin littafin tarihin sarakunan Isra’ila.
35 Yehu ya huta tare da kakanninsa, aka binne shi a Samariya. Yehoyahaz kuma
ya ci sarauta bayansa. 36 Yehu ya yi sarautar Isra’ila a Samariya shekara ashirin da
takwas.

# 11

*Ataliya da Yowash*
*(2 Tarihi 22.10-12)*
1 Da Ataliya mahaifiyar Ahaziya ta ga ɗanta ya mutu, sai ta shiga hallaka dukan
iyalin gidan sarauta. 2 Amma Yehosheba, ’yar Sarki Yoram*, ’yar’uwar Ahaziya, ta
ɗauki Yowash ɗan Ahaziya daga cikin ’ya’yan sarkin da ake shiri a kashe, ta ɓoye.
Ta ɓoye shi daga Ataliya a wurin mai lura da shi a ɗakin kwana; don kada a kashe
shi. 3 Ya kasance a ɓoye, shi da mai lura da shi, a haikalin Ubangiji shekara shida
yayinda Ataliya take mulkin ƙasar.
*(2 Tarihi 23.1-21)*
4 A shekara ta bakwai sai Yehohiyada ya aika a kira komandodin sojoji ɗari-ɗari,
da Keretawa, da matsara, ya sa aka kawo masa su a haikalin Ubangiji. Ya ƙulla
yarjejjeniya da rantsuwa da su a haikalin Ubangiji, sa’an nan ya nuna musu ɗan
sarki. 5 Ya umarce su cewa, “Ga abin da za ku yi sa’ad da kuka zo aiki a Asabbaci, ku
raba kanku kashi uku. Kashi ɗaya za su yi gadin gidan sarki, 6 kashi ɗaya za su yi
gadin Kofar Sur, kashi ɗaya kuma za su yi gadin ƙofar da take bayan ’yan gadin fada.
Dukan waɗannan ƙungiyoyi uku za su yi gadin fadan, 7 ku kuma da kuke a sauran

* 11:2 Da Ibraniyanci Yehoram, wani suna na Yehoram

ƙungiyoyi biyu da kun saba hutu a Asabbaci, duk za ku yi gadin haikali don sarki.
8 Ku tsaya kewaye da sarki, kowane mutum da makaminsa a hannu. Duk wanda ya
kusace ku, ku kashe shi. Ku manne wa sarki duk inda ya tafi."
9 Komandodin sojoji suka yi yadda Yehohiyada firist ya umarta. Kowa ya
ɗauki mutanensa, waɗanda za su kama aiki Asabbaci da waɗanda za su kama
hutun Asabbaci, suka zo wurin Yehohiyada firist. 10 Sai ya ba komandodin māsu
da garkuwoyi da dā suke na Dawuda, waɗanda suke a cikin haikalin UBANGIJI.
11 Matsaran kuma kowa da makaminsa a hannu, suka tsaya kewaye da sarki, kusa
da bagade da kuma haikali, daga gefen kudu zuwa gefen arewa na haikalin.
12 Sai Yehohiyada ya fito da ɗan sarki ya sa masa rawani a kā; ya ba shi shafin
alkawari, ya kuma furta shi sarki. Suka shafe shi da mai, mutane kuma suka yi ta
tafi suka ihu, suna cewa, "Ran sarki yă daɗe."
13 Sa'ad da Ataliya ta ji surutun matsara da na mutane, sai ta tafi wurin mutanen
a haikalin UBANGIJI. 14 Da ta duba sai ga sarki, tsaye kusa da ginshiƙi, bisa ga al'ada.
Hafsoshi da masu busa suna tsaye kusa da sarki, dukan mutanen ƙasar kuma suna
farin ciki suna busa ƙahoni. Sai Ataliya ta keta tufafinta ta tā da murya tana cewa,
"Kai! Wannan cin amana ne! Ai, wannan cin amana ne!"
15 Yehohiyada ya umarci komandodin sojoji waɗanda suke lura da mayaƙa, ya ce,
"Ku fitar da ita daga cikinku, ku kuma kashe duk wanda ya bi ta." Gama firist ɗin ya
ce, "Kada a kashe ta a cikin haikalin UBANGIJI." 16 Saboda haka suka kama ta yayinda
ta kai inda dawakai sukan shiga filin fada, a can kuwa aka kashe ta.
17 Sa'an nan Yehohiyada ya yi alkawari tsakanin UBANGIJI da sarki da kuma mutane
cewa za su zama mutanen UBANGIJI. Ya kuma yi alkawari tsakanin sarki da mutane.
18 Sai dukan mutanen ƙasar suka tafi haikalin Ba'al suka rushe shi. Suka farfasa
bagadai da kuma gumaka, suka kuma kashe Mattan wanda yake firist na Ba'al a
gaban bagade.

Sa'an nan Yehohiyada firist ya sa matsara a haikalin UBANGIJI. 19 Ya tafi tare da
komandodin sojoji, Keretawa, matsara da kuma dukan mutanen ƙasar, tare kuwa
suka kawo sarki daga haikalin UBANGIJI zuwa cikin fada, ta ƙofar matsara. Sarki
kuwa ya ɗauki mazauninsa a bisa kursiyin sarauta, 20 dukan mutanen ƙasar suka yi
murna. Birnin ya sami salama don an kashe Ataliya da takobi a fada.
21 Yowash† yana da shekara bakwai sa'ad da ya fara mulki.

# 12

*Yowash ya gyara haikali*
*(2 Tarihi 24.1-16)*

1 A shekara ta bakwai ta Yehu, Yowash ya zama sarki, ya kuma yi mulki
a Urushalima na tsawon shekaru arba'in. Sunan mahaifiyarsa Zibiya ce; daga
Beyersheba. 2 Yowash ya aikata abin da yake daidai a idon UBANGIJI domin
Yehohiyada firist ya koya masa. 3 Amma fa ba a kawar da masujadan kan tuddai
ba; mutane suka ci gaba da miƙa hadayu da kuma ƙona turare a kan tuddai.
4 Yowash ya ce wa firistoci, "Ku tattara dukan kuɗin da ake kawo a matsayin hadayu
masu tsarki na haikalin UBANGIJI, kuɗin da aka tattara a ƙidaya, kuɗin da aka tattara
daga wa'adin da mutum ya yi, da kuma kuɗin da aka kawo na yardan rai a haikali.
5 Bari kowane firist yă karɓi kuɗi daga masu ajiya, sa'an nan a yi amfani da su a
gyara duk wani abin da ya lalace a haikali."
6 Amma har zuwa shekara ta ashirin da uku ta mulkin Yowash, firistocin ba su yi
gyara haikalin ba. 7 Saboda haka Sarki Yowash ya kira Yehohiyada firist da sauran
firistoci ya tambaye su ya ce, "Me ya sa ba kwa gyaran abubuwan da suka lalace a

† **11:21** Da Ibraniyanci Yehowash, wani suna na Yowash.

haikali? Kada ku sāke karɓan kuɗi daga masu ajiya, amma a miƙa su domin gyaran
haikali.” 8 Firistoci suka yarda cewa ba za su sāke karɓan kuɗi daga mutane ba,
kuma ba za su yi gyaran haikalin da kansu ba.

9 Yehohiyada firist ya ɗauki akwatin ya huda rami a murfinsa. Ya ajiye shi kusa da
bagade a hannun dama na haikalin Ubangiji. Firistocin da suke tsaron ƙofar suka
zuba dukan kuɗin da aka kawo a haikalin Ubangiji a cikin akwatin. 10 Duk sa’ad
da suka ga kuɗin sun ƙaru a akwatin, sai marubucin fada da babban firist, su ƙirga
kuɗin da aka kawo a haikalin Ubangiji su sa a jakankuna. 11 Sa’ad da suka ga kuɗin
ya yi yawa, sai su ba wa waɗanda aka zaɓa su lura da aikin haikalin. Da shi suka
biya waɗanda suka yi aiki a haikalin Ubangiji, su kafintoci, da magina, 12 masu gini,
da masu fasa duwatsu. Suka sayi katakai da sassaƙaƙƙun duwatsu domin gyaran
haikalin Ubangiji, suka kuma biya duk waɗansu kuɗin gyaran haikalin.

13 Ba a yi amfani da kuɗin da aka kawo a haikali don yin manyan kwanonin azurfa,
lagwani, abin yayyafa ruwa, kakaki ko wani abu na zinariya, ko na azurfa domin
haikalin Ubangiji ba; 14 an ba ma’aikatan da suka gyara haikalin ne. 15 Ba su bukaci
wani bayani daga waɗanda aka ba wa kuɗin don su biya ma’aikatan ba, domin sun
yi aikinsu da aminci. 16 Ba a kawo kuɗi daga hadayun laifi da na hadayun zunubi a
haikalin Ubangiji ba, waɗannan na firistoci ne.

17 A wannan lokaci, Hazayel sarkin Aram ya haura, ya kai wa Gat hari, ya kuma
ci ta da yaƙi. Sa’an nan ya juya don yǎ yaƙi Urushalima. 18 Amma Yowash sarkin
Yahuda ya kwashe tsarkakan kayan da kakanninsa, Yehoshafat, Yehoram da Ahaziya,
sarakunan Yahuda suka keɓe, da kyautai da shi kansa ya keɓe, da kuma dukan
azurfan da aka samu a ɗakunan ajiya haikalin Ubangiji da na fada, ya aika da su
wa Hazayel sarkin Aram, shi kuma ya janye daga Urushalima.

19 Game da sauran ayyukan mulkin Yowash da duk abin da ya yi, duk a rubuce suke
a cikin littafin tarihin sarakunan Yahuda. 20 Hafsoshinsa suka yi masa maƙarƙashiya
suka kashe shi a Bet Millo, a kan hanyar da ta gangara zuwa Silla. 21 Hafsoshin da
suka kashe shi kuwa su ne Yozabad ɗan Shimeyat da Yehozabad ɗan Shomer. Ya
mutu, aka kuma binne shi tare da kakanninsa a Birnin Dawuda. Sai Amaziya ɗansa
ya gāje shi a matsayin sarki.

# 13

### *Yehoyahaz sarkin Isra’ila*

1 A shekara ta ashirin da uku ta Yowash ɗan Ahaziya, sarkin Yahuda, Yehoyahaz
ɗan Yehu, ya zama sarkin Isra’ila a Samariya, ya kuwa yi mulki shekaru goma sha
bakwai. 2 Ya aikata mugunta a gaban Ubangiji ta wurin bin zunuban Yerobowam
ɗan Nebat, wanda ya sa Isra’ila ta aikata, bai kuwa guje musu ba. 3 Saboda haka
fushin Ubangiji ya ƙuna a kan Isra’ila, kuma da daɗewa ya sa su a ƙarƙashin ikon
Hazayel sarkin Aram da Ben-Hadad ɗansa.

4 Sai Yehoyahaz ya nemi tagomashin Ubangiji, Ubangiji kuwa ya saurare shi, domin
ya gan irin matsin da sarkin Aram yake yi wa Isra’ila. 5 Sai Ubangiji ya tā da mai
ceto wa Isra’ila, suka kuma kuɓuta daga ikon Aram. Ta haka Isra’ilawa suka yi zama
a gidajensu yadda suka yi a dā. 6 Sai dai ba su bar yin zunuban gidan Yerobowam
ba, wanda ya sa Isra’ila ta aikata; suka ci gaba da yinsu. Haka ma, ginshiƙin Ashera
ta kasance a tsaye a cikin Samariya.

7 Ba abin da ya rage na rundunar Yehoyahaz sai mahayan dawakai hamsin,
kekunan yaƙi goma da kuma sojoji ƙasa dubu goma. Gama sarkin Aram ya hallaka
sauran, ya kuma yi kaca-kaca da su kamar ƙura a masussuka.

8 Game da sauran ayyukan mulkin Yehoyahaz, dukan abubuwan da ya yi da kuma
nasarorinsa, duk a rubuce suke a cikin littafin tarihin sarakunan Isra'ila. 9 Yehoyahaz
ya huta da kakanninsa, aka binne shi a Samariya, Yehowash ɗansa kuma ya gāje shi.

### *Yehowash sarkin Isra'ila*

10 A shekaru talatin da bakwai ta Yowash sarkin Yahuda, Yehowash ɗan Yehoyahaz
ya zama sarkin Isra'ila a Samariya, ya kuma yi mulki shekaru goma sha shida. 11 Ya
aikata mugunta a gaban UBANGIJI, bai juya ga barin zunuban Yerobowam ɗan Nebat
ba, wanda ya sa Isra'ila ta aikata, ya ci gaba da yinsu.
12 Game da sauran ayyukan mulkin Yowash, da dukan abubuwan da ya yi, da kuma
nasarorinsa, haɗe da yaƙin da ya yi da Amaziya sarkin Yahuda, duk a rubuce suke a
cikin littafin tarihin sarakunan Isra'ila. 13 Yowash ya huta da kakanninsa, Yerobowam
kuwa ya gāje shi. Aka binne Yehowash a Samariya tare da sarakunan Isra'ila.
14 To, Elisha ya kamu da ciwon da ya kashe shi. Yowash sarkin Isra'ila ya gangara
don yă gan shi, ya kuma yi kuka dominsa. Ya yi kuka yana cewa, "Babana! Babana,
keken yaƙin Isra'ila da mahayan dawakanta!"
15 Elisha ya ce wa Yehowash, "Ka samo baka da kibiyoyi," ya kuwa yi haka. 16 Sai
ya ce wa Yehowash sarkin Isra'ila, "Ka ɗauki baka a hannunka." Da ya ɗauka, sai
Elisha ya sa hannunsa a hannuwan sarki.
17 Ya ce masa, "Ka buɗe taga wajen gabas," sai ya buɗe. Sai Elisha ya ce, "Ka
harba!" Sai ya harba. Elisha ya ce, "Kibiyar nasara ta UBANGIJI, kibiyar nasara a kan
Aram! Za ka hallaka Arameyawa sarai a Afek."
18 Sa'an nan ya ce, "Ka ɗauki kibiyoyi," sai sarkin ya ɗauko. Sai Elisha ya ce, "Ka
caki ƙasa." Sai ya caka sau uku sa'an nan ya daina. 19 Sai mutumin Allah ya yi fushi
da shi ya ce, "Da a ce ka caki ƙasar sau biyar ko shida; da za ka yi nasara a kan Aram
ka kuma hallaka ta sarai. Amma yanzu za ka yi nasara a kanta sau uku ne kawai."
20 Elisha ya mutu, aka kuma binne shi.
To, mahara Mowabawa sun saba kawo hari a ƙasar Isra'ila a kowace bazara.
21 Wata rana yayinda waɗansu Isra'ilawa suke binne wani mutum, farat ɗaya sai
ga mahara; saboda haka suka jefar da gawar mutumin a kabarin Elisha. Da gawar
ta taɓa ƙasusuwan Elisha, sai mutumin ya farka, ya tashi ya tsaya da ƙafafunsa.
22 Hazayel sarkin Aram ya musguna wa Isra'ila a duk tsawon mulkin Yehoyahaz.
23 Amma UBANGIJI ya nuna musu alheri, ya ji tausayinsu, ya kuma damu da su saboda
alkawarinsa da Ibrahim, Ishaku da Yaƙub. Har yă zuwa yau bai yarda yă hallaka su
ko yă shafe su daga gabansa ba.
24 Hazayel sarkin Aram ya mutu, sai Ben-Hadad ɗansa ya gāje shi. 25 Sa'an nan
Yowash ya sāke ƙwato garuruwan da Ben-Hadad ya ci da yaƙi a hannun mahaifinsa
Yehoyahaz. Sau uku Yehowash ya yi nasara a kansa, ta haka kuwa ya ƙwace
garuruwan Isra'ilawa.

## 14

### *Amaziya sarkin Yahuda*
*(2 Tarihi 25.1-24)*

1 A shekara ta biyu ta mulkin Yehowash ɗan Yehoyahaz sarkin Isra'ila, Amaziya
ɗan Yowash sarkin Yahuda ya fara mulki. 2 Ya zama sarki yana da shekaru ashirin
da biyar, ya kuma yi mulki a Urushalima shekaru ashirin da tara. Sunan mahaifiyarsa
Yehoyaddin, mutuniyar Urushalima. 3 Ya aikata abin da yake daidai a gaban UBANGIJI,
sai dai ba kamar kakansa Dawuda ba. A kome dai ya bi gurbin mahaifinsa Yowash.
4 Ba a dai kawar da masujadan kan tudu ba; mutane suka ci gaba da yin hadaya da
ƙone turare a can.

5 Bayan masarauta ta kahu a hannunsa, sai ya kashe fadawan da suka kashe
mahaifinsa sarki. 6 Duk da haka bai kashe ’ya’yan masu kisan ba, bisa ga abin da yake
a rubuce a Dokar Musa inda UBANGIJI ya umarta, “Ba za a kashe iyaye saboda laifin
’ya’ya ba, ko kuma ’ya’ya saboda laifin iyayensu ba, kowa zai mutu don zunubansa.”[*]
7 Shi ne kuma wanda ya ci mutanen Edom dubu goma a yaƙi, a Kwarin Gishiri, ya
kuma ci Sela da yaƙi, ya ba ta suna Yokteyel, sunan da ake kiranta har wa yau.
8 Sai Amaziya ya aika ’yan aika wurin Yehowash ɗan Yehoyahaz, ɗan Yehu, sarkin
Isra’ila, yana tsokanarsa cewa, “Zo, mu sadu fuska da fuska.”
9 Amma Yehowash sarkin Isra’ila ya mai da martani wa Amaziya sarkin Yahuda
ya ce, “Wata ’yar ƙaya a kurmin Lebanon ta aika da saƙo wurin itacen al’ul a
Lebanon cewa, ‘Ka ba ɗana ’yarka aure.’ Amma wani naman jeji ya zo ya tattake
ƙayar. 10 Tabbatacce ka ci Edom da yaƙi, yanzu kuwa kana ɗaga kai. To, ka gode da
darajar da ka samu, amma ka zauna a gida! Don me kake neman faɗa kana neman
fāɗuwarka da kuma ta Yahuda?”
11 Amma Amaziya bai saurara ba, saboda haka Yehowash sarkin Isra’ila ya kai masa
hari. Shi da Amaziya sarkin Yahuda suka fuskanci juna a Bet-Shemesh. 12 Isra’ila
suka fatattaki Yahuda, kowa kuwa ya tsere zuwa gidansa. 13 Yehowash sarkin Isra’ila
ya kama Amaziya sarkin Yahuda, ɗan Yowash, ɗan Ahaziya, a Bet-Shemesh. Sa’an
nan Yehowash ya tafi Urushalima ya rushe katangar Urushalima daga Kofar Efraim
har zuwa Kofar Kusurwa, ratarta ta kai wajen ƙafa ɗari shida. 14 Ya kwashi ɗaukan
zinariya da azurfa da duk kayan da aka samu a haikalin UBANGIJI da kuma ma’ajin
fadan. Ya kuma kwashi bayi sa’an nan ya koma Samariya.
15 Game da sauran ayyukan mulkin Yehowash, abin da ya yi da kuma nasarorinsa,
haɗe da yaƙinsa da Amaziya sarkin Yahuda, duk a rubuce suke a cikin littafin tarihin
sarakunan Isra’ila. 16 Ya huta da kakanninsa aka kuma binne shi a Samariya tare da
sarakunan Isra’ila. Yerobowam ɗansa, ya kuma gāje shi.
17 Amaziya ɗan Yowash sarkin Yahuda ya yi shekaru goma sha biyar bayan
mutuwar Yehowash ɗan Yehoyahaz sarkin Isra’ila. 18 Game da sauran ayyukan
mulkin Amaziya, duk a rubuce suke a cikin littafin tarihin sarakunan Yahuda.
19 Suka ƙulla masa maƙarƙashiya a Urushalima, ya gudu zuwa Lakish, amma suka
aika har Lakish aka kashe shi a can. 20 Aka ɗauko shi a kan doki aka kawo shi
Urushalima, aka kuwa binne shi tare da kakanninsa, a Birnin Dawuda.
21 Sa’an nan dukan mutanen Yahuda suka ɗauki Azariya,[†] wanda yake ɗan shekaru
goma sha shida da haihuwa, suka naɗa shi sarki a madadin mahaifinsa Amaziya.
22 Shi ne ya sāke gina Elat, ya kuma maido da ita a hannun Yahuda bayan Amaziya
ya huta da kakanninsa.

### *Yerobowam na biyu sarkin Isra’ila*

23 A shekara ta goma sha biyar ta mulkin Amaziya ɗan Yowash sarkin Yahuda,
Yerobowam ɗan Yehowash sarkin Isra’ila ya zama sarki a Samariya, ya kuma yi
mulki na shekaru arba’in da ɗaya. 24 Ya aikata mugunta a gaban UBANGIJI bai kuwa
kauce wa duk zunuban Yerobowam ɗan Nebat, wanda ya sa Isra’ila ta aikata ba.
25 Shi ne ya maido da iyakokin Isra’ila daga Lebo[‡] Hamat zuwa Tekun Araba,[§] bisa
ga maganar UBANGIJI, Allah na Isra’ila, da ya yi ta bakin bawansa Yunana ɗan Amittai,
annabi daga Gat-Hefer.
26 UBANGIJI ya ga irin muguwar wahalar da ta shafi kowa a Isra’ila, ko bawa ko
’yantacce, babu mai taimakonsu. 27 Da yake kuma UBANGIJI bai ce zai shafe sunan
Isra’ila daga fuskar duniya ba, sai ya cece su ta hannun Yerobowam ɗan Yowash.

---

[*] **14:6** M Sh 24.16. [†] **14:21** Wanda ake kuma kira Uzziya [‡] **14:25** Ko kuwa daga mashigin [§] **14:25** Wato, Mataccen Teku

28 Game da sauran ayyukan mulkin Yerobowam, da dukan abin da ya yi, da yaƙe-
yaƙen da ya yi, haɗe da sāke ƙwato wa Isra'ila Damaskus da Hamat waɗanda suke
a hannun Yahuda,* duk a rubuce suke a cikin littafin tarihin sarakunan Isra'ila.
29 Yerobowam ya huta da kakanninsa, sarakunan Isra'ila. Zakariya ɗansa kuwa ya
gāje shi.

# 15

*Azariya sarkin Yahuda*
*(2 Tarihi 26.1-23)*

1 A shekara ta ashirin da bakwai ta mulkin Yerobowam sarkin Isra'ila, Azariya
ɗan Amaziya, sarkin Yahuda ya fara mulki. 2 Yana da shekara goma sha shida sa'ad
da ya zama sarki, ya kuma yi mulki a Urushalima shekara hamsin da biyu. Sunan
mahaifiyarsa Yekoliya daga Urushalima. 3 Ya aikata abin da yake daidai a gaban
UBANGIJI, yadda mahaifinsa Amaziya ya yi. 4 Amma bai kawar da masujadan kan
tudu ba; mutane kuwa suka yi ta yin hadaya da ƙona turare a can.

5 UBANGIJI ya sa wa sarki ciwon kuturta har mutuwarsa, ya kuma zauna a keɓe.*
Yotam ɗan sarki, shi ne ya gudanar da sha'anin fada, ya kuma shugabanci mutanen
ƙasar.

6 Game da sauran ayyukan mulkin Azariya, duk a rubuce suke a cikin littafin tarihin
sarakunan Yahuda. 7 Azariya ya huta tare da kakanninsa, aka kuma binne shi kusa
da su a Birnin Dawuda. Yotam ɗansa, kuma ya gāje shi.

*Zakariya sarkin Isra'ila*

8 A shekara ta talatin da takwas ta mulkin Azariya sarkin Yahuda, Zakariya ɗan
Yerobowam ya zama sarkin Isra'ila a Samariya, ya kuma yi mulki wata shida. 9 Ya
aikata mugunta a gaban UBANGIJI yadda mahaifinsa ya yi. Bai bar aikata zunuban
Yerobowam ɗan Nebat, wanda ya sa Isra'ila suka yi ba.

10 Sai Shallum ɗan Yabesh ya ƙulla wa Zakariya maƙarƙashiya. Ya tasam masa a
gaban jama'a,† ya kashe shi, ya kuma gāje shi. 11 Game da sauran ayyukan mulkin
Zakariya, duk a rubuce suke a cikin littafin tarihin sarakunan Isra'ila. 12 Ta haka
maganar UBANGIJI da ya yi wa Yehu ta cika, wadda ya ce, "Zuriyarka za tă zauna a
kursiyin Isra'ila har tsara ta huɗu."‡

*Shallum sarkin Isra'ila*

13 Shallum ɗan Yabesh ya zama sarki a shekara ta talatin da tara ta mulkin Uzziya
sarkin Yahuda, ya kuma yi mulki na wata ɗaya a Samariya. 14 Sa'an nan Menahem
ɗan Gadi ya gangara daga Tirza ya haura zuwa Samariya. Ya tasam wa Shallum ɗan
Yabesh a Samariya, ya kashe shi, ya kuma gāje shi.

15 Game da sauran ayyukan mulkin Shallum, duk a rubuce suke a cikin littafin
tarihin sarakunan Isra'ila.

16 A lokacin nan sai Menahem ya taso daga Tirza, ya kai wa Tifsa hari da kowa
wanda yake a birnin da kewayenta, don sun ƙi su buɗe ƙofofinsu. Ya kori Tifsa daga
aiki, ya kuma tsattsaga cikin dukan mata masu juna biyu.

*Menahem sarkin Isra'ila*

17 A shekara ta talatin da takwas ta mulkin Azariya sarkin Yahuda, Menahem
ɗan Gadi ya zama sarkin Isra'ila, ya yi mulki a Samariya shekara goma. 18 Ya
aikata mugunta a gaban UBANGIJI. A duk tsawon mulkinsa, bai rabu da zunuban
da Yerobowam ɗan Nebat ya sa Isra'ila suka aikata ba.

---

* **14:28** Ko kuwa Yahuda * **15:5** Ko kuwa a gidan da aka fisshe shi daga ɗauka ɗawainiya † **15:10** Da Ibraniyanci; waɗansu rubuce-rubucen hannu na Seftuwajin suna da in Ibileyam ‡ **15:12** 2Sar 10.30.

19 Sai Ful§ sarkin Assuriya ya kai wa ƙasar hari, Menahem kuwa ya ba shi talenti
dubu na azurfa don yǎ sami goyon bayansa, yǎ kuma ƙarfafa kahuwa mulkin.
20 Menahem ya tara kuɗin ne ta hanyar haraji a Isra'ila inda ya sa kowane attajiri ya
ba da shekel hamsin don a ba sarkin Assuriya. Sa'an nan sarkin Assuriya ya janye,
bai ƙara kasance a ƙasar ba.
21 Game da sauran ayyukan mulkin Menahem, duk a rubuce suke a cikin littafin
tarihin sarakunan Isra'ila. 22 Menahem ya huta tare da kakanninsa. Fekahiya ɗansa
kuma ya gāje shi.

### Fekahiya sarkin Isra'ila

23 A shekara ta hamsin ta mulkin Azariya sarkin Yahuda, Fekahiya ɗan Menahem
ya zama sarkin Isra'ila a Samariya, ya kuma yi mulki shekara biyu. 24 Fekahiya
ya aikata mugunta a gaban Ubangiji, bai rabu da zunuban Yerobowam ɗan Nebat
wanda ya sa Isra'ila ya aikata ba. 25 Ɗaya daga cikin manyan fadawansa, Feka ɗan
Remaliya, ya ƙulla masa maƙarƙashiya. Ɗauke da mutanen Gileyad hamsin, ya
kashe Fekahiya tare da Argob da kuma Ariye a fadan sarki a Samariya. Ta haka Feka
ya kashe Fekahiya ya kuma gāje shi.
26 Game da sauran ayyukan mulkin Fekahiya, duk a rubuce suke a cikin littafin
tarihin sarakunan Isra'ila.

### Feka sarkin Isra'ila

27 A shekara ta hamsin da biyu ta mulkin Azariya sarkin Yahuda, Feka ɗan Remaliya
ya zama sarkin Isra'ila a Samariya, ya yi mulki shekara ashirin. 28 Ya aikata mugunta
a gaban Ubangiji. Bai kauce wa zunuban Yerobowam ɗan Nebat, wanda ya sa Isra'ila
ta yi ba.
29 A zamanin Feka sarkin Isra'ila, Tiglat-Fileser sarkin Assuriya ya zo ya kama
Iyon, Abel-Bet-Ma'aka, Yanowa da Kedesh da kuma Hazor. Ya kame Gileyad da Galili,
haɗe da dukan ƙasar Naftali, ya kuma kwashi mutanen zuwa Assuriya. 30 Sa'an nan
Hosheya ɗan Ela ya ƙulla wa Feka ɗan Remaliya maƙarƙashiya. Ya fāɗa masa ya
kuma kashe shi, sa'an nan ya gāje shi a matsayin sarki a shekara ta shirin ta mulkin
Yotam ɗan Uzziya.
31 Game da sauran ayyukan mulkin Feka da duk abin da ya yi, duk a rubuce suke
a cikin littafin tarihin sarakunan Isra'ila.

### Yotam sarkin Yahuda
### (2 Tarihi 27.1-9)

32 A shekara ta biyu ta mulkin Feka ɗan Remaliya sarkin Isra'ila, Yotam ɗan Uzziya
sarkin Yahuda ya fara mulki. 33 Ya zama sarki yana da shekara ashirin da biyar, ya
kuma yi mulki a Urushalima shekara goma sha shida. Sunan mahaifiyarsa Yerusha,
'yar Zadok. 34 Ya aikata abin da yake daidai a gaban Ubangiji yadda mahaifinsa
Uzziya ya yi. 35 Duk da haka, bai kawar da masujadan kan tudu ba; mutane suka ci
gaba da yin hadaya da ƙona turare a can. Yotam ya sāke gina Kofar Bisa ta haikalin
Ubangiji.
36 Game da sauran ayyukan mulkin Yotam da aikin da ya yi, duk a rubuce suke a
cikin littafin tarihin sarakunan Yahuda. 37 (A kwanakin nan Ubangiji ya fara aikan
Rezin sarkin Aram da Feka ɗan Remaliya, su yi gāba da Yahuda.) 38 Yotam ya huta tare
da kakanninsa, aka kuma binne shi tare da su a Birnin Dawuda, birnin mahaifinsa.
Ahaz ɗansa kuma ya gāje shi.

§ **15:19** Wanda kuma ake kira Tiglat-Fileser

# 16

### *Ahaz sarkin Yahuda*
### *(2 Tarihi 28.1-27)*

1 A shekara ta goma sha bakwai ta mulkin Feka ɗan Remaliya, Ahaz ɗan Yotam
sarkin Yahuda ya fara mulki. 2 Ahaz ya zama sarki yana da shekara ashirin, ya
kuma yi mulki shekara goma sha shida a Urushalima ba kamar Dawuda mahaifinsa
ba. Ahaz bai yi abin da yake daidai a gaban UBANGIJI Allahnsa ba. 3 Ya yi tafiya a
hanyoyin sarakunan Isra'ila har ya miƙa ɗansa hadaya a[*] wuta, yana bin hanyoyin
banƙyama na al'ummai da UBANGIJI ya kora a gaban Isra'ilawa. 4 Ya miƙa hadaya, ya
kuma ƙona turare a masujadan tudu, da kan tuddai, da kuma a ƙarƙashin kowane
babban itace.

5 Sai Rezin sarkin Aram, da Feka ɗan Remaliya sarkin Isra'ila suka haura don su
kai wa Urushalima hari, suka kuma kewaye Ahaz, amma ba su iya shan ƙarfinsa ba.
6 A wannan lokaci, Rezin sarkin Aram ya sāke ƙwato Elat wa Aram ta wurin korar
Yahuda. Sa'an nan mutanen Edom suka mamaye Elat suna kuwa zaune a can har
yau.

7 Ahaz ya aika a faɗa wa Tiglat-Fileser sarkin Assuriya cewa, "Ni abokin tarayyarka
ne kuma mai dogara da kai. Ka haura ka cece ni daga hannun sarkin Aram da hannun
sarkin Isra'ila waɗanda suke kawo mini hari." 8 Ahaz ya ɗauki azurfa da zinariyar
da suke a haikalin UBANGIJI da suke kuma a ma'ajin fada ya aika wa sarkin Assuriya
kyauta. 9 Sai sarkin Assuriya ya ji roƙonsa. Ya tashi ya fāɗa wa Damaskus da hari
ya kuma kame ta. Ya kwashi mazaunanta zuwa Kir, ya kuma kashe Rezin.

10 Sa'an nan sarki Ahaz ya tafi Damaskus don yă sadu da Tiglat-Fileser sarkin
Assuriya. Da ya kai can sai ya ga wani bagade a Damaskus, sai ya aika wa Uriya
firist, da siffar bagaden, da fasalinsa, da cikakken bayanin bagaden. 11 Saboda haka
Uriya firist ya gina bagaden bisa ga tsarin da Sarki Ahaz ya aika masa daga Damaskus,
ya kuma gama shi kafin Sarki Ahaz yă dawo. 12 Da sarki ya dawo daga Damaskus
ya ga bagaden, sai ya tafi kusa da shi ya kuma miƙa hadaya[†] a bisansa. 13 Ya miƙa
hadayarsa ta ƙonawa da ta hatsi, ya zuba hadayarsa ta sha, ya kuma yayyafa jinin
hadayunsa ta zumunci a bisa bagaden. 14 Sai ya cire bagaden tagulla wanda aka keɓe
ga UBANGIJI, ya sa shi a gaban haikalin wato, tsakanin ƙofar shiga haikalin UBANGIJI
da sabon bagaden. Ya ajiye shi a gefen arewa na sabon bagaden.

15 Sarkin Ahaz ya umarci Uriya cewa, "A kan babban sabon bagade, ka miƙa
hadayar ƙonawa ta safe, da hadayar hatsi ta yamma, da hadayar sarki ta ƙonawa da
hadayarsa ta hatsi, da hadaya ta dukan jama'ar ƙasar, tare da hadayan hatsinsu da
kuma ta sha. Ka yayyafa jinin hadayun ƙonawa a kan bagade. Amma zan yi amfani
da bagaden tagulla don neman bishewa." 16 Uriya firist kuwa ya yi duk abin da Sarki
Ahaz ya umarta.

17 Sarkin Ahaz ya kawar da katakon ya kuma ɗauke tasoshin daga mazauninsu da
ake iya matsarwa. Ya ɗauke ƙaton kwano mai suna Teku daga kan bijiman tagullar
da ya tallafe su ya ajiye a kan mazaunin dutse. 18 Ya kawar da rumfa Asabbacin da
aka gina a haikalin, ya kuma kawar da mashigin sarki na waje da haikalin UBANGIJI,
duk dai don yă gamshi sarkin Assuriya.

19 Game da sauran ayyukan mulkin Ahaz, abubuwan da ya yi, duk a rubuce suke
a cikin littafin tarihin sarakunan Yahuda. 20 Ahaz ya huta tare da kakanninsa, aka
kuma binne shi da su a Birnin Dawuda. Hezekiya ɗansa kuma ya gāje shi.

---

[*] **16:3** Ko kuwa ya ma sa ɗansa ya ratsa [†] **16:12** Ko kuwa ya kuma haura

# 17

### *Hosheya sarkin Isra'ila na ƙarshe*

[1] A shekara ta goma sha biyu ta mulkin Ahaz sarkin Yahuda, Hosheya ɗan Ela
ya zama sarkin Isra'ila a Samariya, ya kuma yi mulki na shekara tara. [2] Ya aikata
mugunta a gaban UBANGIJI, amma ba kamar na sarakunan Isra'ilan da suka riga shi
ba.
[3] Shalmaneser sarkin Assuriya ya kawo wa Hosheya wanda dā abokin tarayyarsa
ne, hari har Hosheya ya biya shi haraji. [4] Amma sarkin Assuriya ya gane cewa
Hosheya mai cin amana ne, gama ya aika da wakilai wurin So* sarkin Masar, ya
kuma daina aika wa sarkin Assuriya haraji yadda ya saba yi kowace shekara. Saboda
haka Shalmaneser ya kama shi ya sa a kurkuku. [5] Sarkin Assuriya ya kai wa ƙasar
Hosheya gaba ɗaya farmaki, ya kewaye Samariya na tsawon shekara uku. [6] A shekara
ta tara ta sarautar Hosheya, sarkin Assuriya ya ci Samariya da yaƙi ya kuma kwashe
Isra'ilawa zuwa Assuriya. Ya tsugunar da su a Hala, da a Gozan a bakin Kogin Habor
da kuma a garuruwan Medes.

### *Isra'ila ya tafi zaman bauta saboda zunubi*

[7] Duk wannan ya faru ne saboda Isra'ilawa sun yi wa UBANGIJI Allahnsu zunubi,
shi wanda ya fitar da su daga Masar daga ƙarƙashin ikon Fir'auna sarkin Masar. Sun
yi wa waɗansu alloli sujada [8] suka kuma bi gurbin al'umman da UBANGIJI ya kora
a gabansu, da kuma ayyukan da sarakuna Isra'ila suka gabatar. [9] Isra'ilawa a ɓoye
sun aikata abubuwan da ba daidai ba ga UBANGIJI Allahnsu. Tun daga hasumiyoyi
har zuwa birane masu katanga, sun gina wa kansu wuraren sujada na tudu a dukan
garuruwansu. [10] Suka kafa keɓaɓɓun duwatsu da kuma ginshiƙan Ashera a kowane
tudu mai tsayi da kuma a ƙarƙashin kowane babban itace. [11] Suka ƙona turare a kan
kowane tudu, kamar dai yadda al'umman da UBANGIJI ya kora daga gabansu suka
yi. Suka yi muguntan da ya sa UBANGIJI ya yi fushi. [12] Suka bauta wa gumaka, ko
da yake UBANGIJI ya ce, "Ba za ku yi wannan ba."† [13] UBANGIJI ya yi wa Isra'ila da
Yahuda kashedi ta bakin dukan annabawansa da kuma masu duba, cewa, "Ku juyo
daga mugayen ayyukanku. Ku yi biyayya da umarnai da farillaina, bisa ga dukan
Dokar da na dokaci kakanninku su bi, waɗanda na kuma bayar ta wurin bayina,
annabawa."
[14] Amma ba su saurare ni ba don sun kangare kamar kakanninsu, waɗanda ba su
amince da UBANGIJI Allahnsu ba. [15] Suka yi watsi da farillansa da yarjejjeniyar da
ya ƙulla da kakanninsu, da kuma kashedin da ya yi musu. Suka bi gumaka marasa
amfani, wannan ya sa su ma kansu suka zama marasa amfani. Suka kwaikwayi
sauran ƙasashen da suke kewaye da su, ko da yake UBANGIJI ya umarce su cewa,
"Kada ku yi rayuwa irin tasu," suka kuwa yi abin da UBANGIJI ya hana su.
[16] Suka wofinta dukan umarnan UBANGIJI Allahnsu, suka yi wa kansu gumakan zubi
na siffar 'yan maruƙa biyu, da kuma ginshiƙin Ashera. Suka rusuna wa rundunan
taurari, suka kuma yi wa Ba'al sujada. [17] Suka miƙa 'ya'yansu maza da mata hadaya
ta‡ wuta. Suka yi duba, suka yi sihiri suka kuma ba da kansu ga mugunta a gaban
UBANGIJI; suka sa ya yi fushi.
[18] Saboda haka UBANGIJI ya yi fushi ƙwarai da Isra'ila, ya kuma kawar da su daga
gabansa. Kabilar Yahuda kaɗai aka bari, [19] ko Yahuda ma ba su kiyaye umarnan
UBANGIJI Allahnsu ba. Sun bi gurbin da Isra'ila ta kawo. [20] Saboda haka UBANGIJI ya
wofinta mutanen Isra'ila; ya azabtar da su, ya kuma ba da su a hannun masu kwasar
ganima, sai da ya shafe su ƙaƙaf daga gabansa.

* **17:4** Ko kuwa wajen Sayis, zuwa ga; So wani mai yiwuwa gajeren suna na Osorkon. † **17:12** Fit 20.4,5.
‡ **17:17** Ko kuwa Suka sa 'ya'yansu maza da mata suka ratsa

21 Sa'ad da ya ware Isra'ila daga gidan Dawuda, sai suka naɗa Yerobowam ɗan
Nebat sarki a kansu. Yerobowam ya rinjayi Isra'ila daga ƙin UBANGIJI, ya sa suka
aikata babban zunubi. 22 Isra'ila suka nace cikin dukan zunuban Yerobowam, ba su
kuwa rabu da su ba 23 har UBANGIJI ya kawar da su daga gabansa, kamar yadda ya
gargaɗe su ta bakin bayinsa annabawa. Saboda haka aka kwashi mutanen Isra'ila
daga ƙasarsu zuwa bauta a Assuriya, har wa yau kuwa suna can.

*An sāke tsugunar da Samariya*

24 Sarkin Assuriya ya kawo mutane daga Babilon, Kuta, Afa, Hamat da Sefarfayim
ya zaunar da su a garuruwan Samariya don su maya gurbin Isra'ilawa. Suka mallaki
Samariya suka kuma zauna a garuruwansu. 25 Sa'ad da suka fara zama a can, ba
su bauta wa UBANGIJI ba; saboda haka ya aika da zakoki a tsakaninsu suka karkashe
waɗansu mutane. 26 Sai aka faɗa wa sarkin Assuriya cewa, "Mutanen da ka kwashe
ka zaunar a garuruwan Samariya fa ba su san abin da allahn ƙasar yake bukata
ba. Saboda haka allahn ƙasar ya tura zakoki a cikinsu, waɗanda suke karkashe su,
domin mutanen ba su san abin da yake bukata ba."

27 Sai sarkin Assuriya ya ba da umarni cewa, "A sami wani daga cikin firistocin da
aka kwaso zuwa bauta daga Samariya, yă koma yă zauna a can, yă koya wa mutanen
abin da allahn ƙasar yake bukata." 28 Saboda haka ɗaya daga cikin firistocin da aka
kawo bauta daga Samariya ya dawo ya zauna a Betel, ya koya musu yadda za su yi
sujada ga UBANGIJI.

29 Duk da haka, jama'ar kowace ƙasa, suka ƙera tasu alloli a garuruwa masu
yawa inda suke zaune, suka sa su a masujadan da mutanen Samariya suka gina
a kan tuddai. 30 Mutane daga Babilon suka ƙera Sukkot Benot, mutane daga Kut
suka ƙera Nergal, mutane daga Hamat suka ƙera Ashima; 31 Awwiyawa suka ƙera
Nibhaz da Tartak, Sefarfayawa kuwa suka ƙone 'ya'yansu a wuta a matsayi hadayu ga
Adrammelek da Anammelek allolin Sefarfayim. 32 Sun yi wa UBANGIJI sujada, amma
kuma suka zaɓi mutanensu su yi musu hidima a matsayin firistoci a masujadan da
suke kan tuddai. 33 Sun yi wa UBANGIJI sujada, amma kuma sun bauta wa allolinsu
bisa ga al'adun ƙasashen da suka fito.

34 Har yă zuwa yau, sun nace da ayyukansu na dā. Ba sa yin wa UBANGIJI sujada, ba
sa kuma bin dokoki da farillansa, dokoki da umarnan da UBANGIJI ya ba wa zuriyar
Yaƙub, wadda ya ba wa suna Isra'ila. 35 Da UBANGIJI ya ƙulla alkawari da Isra'ilawa,
ya dokace su cewa, "Kada ku yi wa waɗansu alloli sujada ko ku durƙusa a gabansu
ku bauta musu, ko ku miƙa musu hadaya. 36 Amma UBANGIJI wanda ya fito da ku
daga Masar da iko mai girma da hannu mai ƙarfi, shi ne za ku yi masa sujada. Gare
shi za ku durƙusa ku kuma miƙa masa hadayu. 37 Dole kullum ku mai da hankali ga
kiyaye ƙa'idodi da farillan, dokoki da umarnan da ya rubuta muku. Kada ku yi wa
waɗansu alloli sujada. 38 Kada ku manta da alkawarin da na ƙulla da ku, kada ku yi
sujada ga waɗansu alloli. 39 Maimakon haka, ku yi wa UBANGIJI Allahnku sujada; shi
ne zai cece ku daga hannun abokan gābanku."

40 Amma ba su saurara ba, suka nace da ayyukansu na dā. 41 Ko ma yayinda
mutanen nan suke yi wa UBANGIJI sujada, ba su daina bauta wa gumakansu ba. Har
yă zuwa yau, 'ya'yansu da jikokinsu sun ci gaba da bin gurbin kakanninsu.

# 18

*Hezekiya sarkin Yahuda*
*(2 Tarihi 29.1,2; 31.1)*

1 A shekara ta uku ta mulkin Hosheya ɗan Ela sarkin Isra'ila, Hezekiya ɗan Ahaz
sarkin Yahuda ya fara mulki. 2 Yana da shekara ashirin da biyar da ya zama sarki, ya

kuma yi mulki shekara ashirin da tara a Urushalima. Sunan mahaifiyarsa Abiya* 'yar
Zakariya. 3 Ya aikata abin da yake daidai a gaban UBANGIJI yadda kakansa Dawuda
ya yi. 4 Ya kawar da masujadan kan tudu, ya farfasa keɓaɓɓun duwatsu, ya sassare
ginshiƙan Ashera. Ya fashe macijin tagullan da Musa ya yi, gama har zuwa lokacin
nan Isra'ilawa suna ƙona turare gare shi. (An ba shi suna Nehushtan.)
5 Hezekiya ya dogara ga UBANGIJI, Allah na Isra'ila. Ba a yi wani kamar sa ba cikin
dukan sarakunan Yahuda; ko kafin shi, ko kuma bayansa. 6 Ya manne wa UBANGIJI,
bai fasa binsa ba; ya yi biyayya da dokokin da UBANGIJI ya ba wa Musa. 7 UBANGIJI
kuma ya kasance tare da shi, ya yi nasara a duk abin da ya sa hannu. Ya yi tawaye
ga sarkin Assuriya, ya ƙi yă bauta masa. 8 Daga hasumiya zuwa birni mai katanga,
ya ci Filistiyawa da yaƙi, har zuwa Gaza da kewaye.
9 A shekara ta huɗu ta Hezekiya, wato, shekara ta bakwai ke nan ta mulkin Hosheya
ɗan Ela sarkin Isra'ila; Shalmaneser Sarkin Assuriya ya tasam ma Samariya da
yaƙi; ya kewaye ta. 10 A ƙarshen shekara ta uku, Assuriyawa suka ci Samariya da
yaƙi. An ci Samariya da yaƙi a shekara ta shida ta mulki Hezekiya, wanda ya zo
daidai da shekara ta tara ta mulkin Hosheya sarkin Isra'ila. 11 Sarkin Assuriya ya
kwashe Isra'ila zuwa Assuriya ya zaunar da su a Hala, da Gozan a kogin Habor da
kuma garuruwan Medes. 12 Wannan ya faru ne domin ba su yi biyayya ga UBANGIJI
Allahnsu ba, amma suka karya alkawarinsu; da dukan abin da Musa bawan UBANGIJI
ya umarta. Ba su saurari umarnin ba, balle su kiyaye su.

*(2 Tarihi 32.1-19; Ishaya 36.1-22)*

13 A shekara ta goma sha huɗu ta mulkin sarkin Hezekiya, sai sarki Sennakerib
sarkin Assuriya ya kai farmaki wa biranen Yahuda masu katanga ya kuma kama su.
14 Sai Hezekiya sarkin Yahuda ya aika saƙo ga sarkin Assuriya a Lakish cewa, "Na
yi laifi, ka janye daga gare ni, zan kuma biya ka duk abin da ake bukata daga gare
ni." Sarkin Assuriya ya karɓi talenti ɗari uku na azurfa, da talenti talatin na zinariya
daga hannun Hezekiya sarkin Yahuda. 15 Ya zama kuwa cewa, Hezekiya ya bayar da
dukan azurfan da suke a haikalin UBANGIJI da kuma a ma'ajin fadan sarki.
16 A wannan lokaci ne Hezekiya sarkin Yahuda ya ɓaɓɓalle zinariyan da aka dalaye
ƙofofi da madogaran ƙofofin haikalin UBANGIJI, ya ba sarkin Assuriya.

### *Sennakerib ya yi wa Urushalima barazana*

17 Sai sarkin Assuriya ya aika da babban shugaban sojojinsa, da shugaban
dattawansa, da wakilinsa daga birnin Lakish tare da ƙungiyar sojoji masu yawa zuwa
Urushalima domin su yaƙi Sarki Hezekiya. Da suka haura sai suka tsaya a wurin
lambatun da yake kawo ruwa daga Tafkin Tudu, kusa da hanyar Filin Mai Wanki.
18 Suka kira sarki, sai Eliyakim ɗan Hilkiya sarkin fada, da Shebna magatakarda, da
Yowa ɗan Asaf marubuci suka je wurinsu.
19 Jagoran dogarawan sarkin Assuriya ya ce musu, "Ku ce wa Hezekiya,
" 'Ga abin da babban sarkin Assuriya ya ce, da wa kake taƙama? 20 Ka ce kana
da dabara da ƙarfin soji, amma bagu kawai kake yi. Da wa ka dogara har da za
ka yi mini tawaye? 21 Na sani kana dogara da Masar, wadda take kamar karar
masara, wadda in ka jingina a kai, za tă karye tă soki hannunka. Haka Fir'auna
sarkin Masar yake ga dukan wanda ya dogara da shi. 22 Sai ya ci gaba da cewa,
in kuma ka ce mini "Muna dogara ga UBANGIJI Allahnmu ne," ba masujadansa da
bagadansa ne Hezekiya ya ciccire, yana ce wa Urushalima da Yahuda, "Dole ku yi
sujada a gaban wannan bagade a Urushalima"?
23 " 'Yanzu, ka zo ku shirya da shugabana, sarkin Assuriya. Zan ba ka dawakai
dubu biyu, in za ka sami mahayansu! 24 Yaya za ka yi tsayayya da mafi ƙanƙantan

---

* **18:2** Da Ibraniyanci Abi, wani sunan Abiya.

hafsan shugabana, ko da kana dogara da Masar don kekunan yaƙi da mahaya
dawakai? 25 Ban da haka ma, kana gani cewa na zo in hallaka wannan wuri ne
ba tare da na ji daga UBANGIJI ba? UBANGIJI da kansa ne ya ce da ni in kawo wa
wannan ƙasa hari in hallaka ta.' "
26 Sai Eliyakim ɗan Hilkiya, da Shebna, da Yowa suka ce wa jagoran dakarun,
"Muna roƙonka ka yi wa bayinka magana da harshen Arameyik da yake muna ji.
Kada ka yi mana magana da Yahudanci domin kada mutanen da suke bisa katanga
su ji!"
27 Amma shugaban sojojin ya ce, "Ai, ba gare ku da sarkinku kaɗai ne shugabana
ya aike ni ba. Amma har ga mutanen da suke zaune a kan katangar birnin, waɗanda
za su ci kashinsu, su sha fitsarinsu!"
28 Sai shugaban sojojin ya yi kira da Yahudanci ya ce, "Ku ji muryar babban sarki,
sarkin Assuriya! 29 Ga abin da sarki ya faɗa; kada ku bar Hezekiya yă ruɗe ku. Ba
zai iya cetonku daga hannuna ba. 30 Kada ku yarda Hezekiya yă rinjaye ku cewa ku
dogara ga Allah, sa'ad da ya ce da ku, 'Ba shakka UBANGIJI zai cece mu; yana ce da
ku birnin nan ba zai faɗa a hannun sarkin Assuriya ba.'
31 "Kada ku saurari Hezekiya. Ga abin da sarkin Assuriya ya ce, ku shirya zaman
lafiya da ni, ku fito zuwa wurina. Kowane ɗayanku kuwa zai ci 'ya'yan inabinsa
da 'ya'yan ɓaurensa, yă kuma sha ruwa daga randarsa, 32 har lokacin da zan zo in
kwashe ku, in kai ku wata ƙasa mai kama da taku, ƙasa mai yalwar hatsi, da ruwan
inabi, da abinci, da gonakin inabi, da itatuwan zaitun, da zuma, don ku rayu, kada
ku mutu!
"Kada ku saurari Hezekiya, don karya yake muku, sa'ad da ya ce, 'UBANGIJI zai cece
mu.' 33 Akwai allahn wata al'ummar da ya taɓa ceton ƙasarsa daga hannun sarkin
Assuriya? 34 Ina allolin Hamat da na Arfad? Ina allolin Sefarfayim, da na Hena, da
na Iffa? Sun cece Samariya daga hannuna? 35 Wanne a cikin dukan allolin ƙasashen
nan ya iya ceton ƙasarsa da gare ni? Shugaban sojojin ya kuma ci gaba da cewa, ta
yaya UBANGIJI zai ceci Urushalima daga hannuna?"
36 Amma mutane suka yi shiru ba su amsa masa ba, domin sarki ya umarta cewa,
"Kada ku amsa masa."
37 Sai Eliyakim ɗan Hilkiya, sarkin fada, da Shebna magatakarda, da Yowa ɗan
Asaf, marubuci, suka je wurin Hezekiya da tufafinsu a kece, suka faɗa masa abin da
shugaban sojojin ya faɗa.

# 19

*An yi annabcin ceton Urushalima*
*(Ishaya 37.1-13)*

1 Da sarki Hezekiya ya ji haka, sai ya kyakketa tufafinsa, ya sa tufafin makoki,
ya shiga haikalin UBANGIJI. 2 Ya aiki Eliyakim sarkin fada, Shebna marubuci da
shugabannin firistoci, dukansu sanye da tufafin makoki, zuwa wurin annabi Ishaya
ɗan Amoz. 3 Suka ce masa, "Hezekiya ya ce, yau ranar wahala ce, da ta cin mutunci,
da ta shan kunya, ga shi, 'ya'ya suna gab da a haife su, amma ba ƙarfin da za a yi
yunƙuri a haife su. 4 Mai yiwuwa UBANGIJI Allahnka ya ji dukan maganganun sarkin
yaƙi, wanda maigidansa, sarkin Assuriya, ya aiko don yă rena Allah mai rai. Bari
UBANGIJI Allahnka yă tsawata masa saboda maganar da ya ji. Saboda haka ka yi
addu'a domin raguwar da har yanzu suke a raye."
5 Da fadawan sarki Hezekiya suka isa wurin Ishaya, 6 Ishaya ya ce musu, "Ku faɗa
wa maigidanku, in ji UBANGIJI, 'Kada abin da ka ji yă firgita ka, wato, waɗannan
kalmomin da karen nan na sarkin Assuriya ya yi saɓo da su. 7 Saurara! Zan sa masa

wani ruhun da zai sa yǎ ji wata jita-jitar da za tǎ sa yǎ koma ƙasarsa. A can zan sa a kashe shi da takobi a ƙasarsa.' "

8 Da sarkin yaƙin ya ji cewa sarkin Assuriya ya bar Lakish, sai ya janye, ya kuma iske sarkin yana yaƙi da Libna.

9 To, Sennakerib ya sami labari cewa Tirhaka, mutumin Kush* sarkin Masar, yana zuwa masa da yaƙi. Saboda haka ya sāke aika manzanni zuwa wurin Hezekiya cewa,
10 "Ku faɗa wa Hezekiya sarkin Yahuda, kada ka bar allahn da kake dogara gare shi yǎ ruɗe ka cewa, 'Urushalima ba za tǎ fāɗi a hannun sarkin Assuriya ba.' 11 Ba
shakka ka riga ka ji abin da sarkin Assuriya ya yi da dukan ƙasashe, yana hallaka su gaba ɗaya. Kai kuwa kana ji za a cece ka? 12 Allolin al'umman da kakannina suka
hallaka, sun cece su ne, allolin Gozan, da na Haran, da na Rezef, da kuma na mutane Eden da suke a Tel Assar? 13 Ina sarkin Hamat, da sarkin Arfad, da sarkin birnin
Sefarfayim, ko na Hena da kuma na Iffa?"

### *Addu'ar Hezekiya*
### *(Ishaya 37.14-20)*

14 Hezekiya ya karɓi wasiƙar daga manzannin ya karanta. Sa'an nan ya tashi ya tafi haikalin UBANGIJI ya shimfiɗa wasiƙar a gaban UBANGIJI. 15 Hezekiya kuwa ya yi
addu'a ga UBANGIJI ya ce, "Ya UBANGIJI, Allah na Isra'ila, wanda yake zaune tsakanin kerubobi, kai kaɗai ne Allah bisa dukan mulkokin duniya. Kai ka yi sama da duniya.
16 Ka kasa kunne, ya UBANGIJI, ka ji; ka buɗe idanunka ya UBANGIJI ka gani; ka saurari kalmomin da Sennakerib ya aiko don yǎ yi wa Allah mai rai ba'a.

17 "Da gaske ne, ya UBANGIJI, cewa sarakunan Assuriya sun hallakar da waɗannan al'ummai da ƙasashensu. 18 Sun jefar da allolinsu cikin wuta, suka hallaka su, gama
ba alloli ba ne, katakai ne da kuma duwatsu, ayyukan hannuwan mutane. 19 To, ya
UBANGIJI Allahnmu, ka cece mu daga hannunsa, don dukan mulkokin duniya su san cewa kai kaɗai, ya UBANGIJI ne Allah."

### *Ishaya ya yi annabcin fāɗuwar Sennakerib*
### *(Ishaya 37.21-35)*

20 Sai Ishaya ɗan Amoz ya aika da saƙo zuwa wurin Hezekiya cewa, "Ga abin da UBANGIJI, Allah na Isra'ila ya ce, na ji addu'arka game da Sennakerib sarkin Assuriya.
21 Ga abin da UBANGIJI yana cewa game da shi,

" 'Budurwar Sihiyona
ta rena ka tana kuma yin maka ba'a.
Diyar Urushalima
ta kaɗa kanta yayinda kake gudu.
22 Wane ne ka zaga, ka kuma yi masa saɓo?
Wa kake gāba da shi har ka ɗaga muryarka,
har ka tā da idanunka da fahariya?
Kana gāba da Mai Tsarki na Isra'ila!
23 Ta wurin manzanninka
ka tara wa UBANGIJI zagi.
Ka kuma ce,
"Da yawa kekunan yaƙina
na haye kan ƙwanƙolin duwatsu,
wurin mafi tsawo na Lebanon.
Na sassare itacen al'ul nasa mafi tsawo
mafi daraja na itacen fir nasa.
Na ratsa har can tsakiyar kurmi,
mafi kyau na kurminsa.

* **19:9** Wato, daga yanki bisa Nilu

24 Na tona rijiyoyi a ƙasashen waje
na kuma sha ruwa a can.
Da tafin ƙafafuna
na busar da dukan rafuffukan Masar."

25 " 'Ba ka taɓa ji ba?
Tun da daɗewa na ƙaddara haka.
Tuntuni kuwa na shirya shi;
yanzu kuma na sa ya faru,
cewa ka mai da birane masu katanga
tarin duwatsu.
26 Karfin mutanensu ya tsiyaye,
suka razana aka kuma kunyata su.
Suna kama da tsirai a gona,
kamar sabon toho
kamar ciyawa mai tohuwa bisa rufin ɗaki
wanda ya bushe saboda zafi, kafin yă yi girma.

27 " 'Amma na san wurin zamanka
da fitarka da shigarka
da yadda kake fushi da ni.
28 Domin kana fushi da ni
reninka ya iso kunnuwata,
zan sa ƙugiyata a hancinka
da linzamina a bakinka,
zan kuma sa ka koma
a ta hanyar da ka zo.'
29 "Wannan zai zama alama a gare ka, ya Hezekiya,
"Bana, za ku ci amfanin gonar da ya tsira da kansa,
baɗi kuma amfanin gonar da ya tsiro daga na bara.
Amma a shekara ta uku, za ku yi shuki, ku kuma girbe,
ku dasa gonakin inabi, ku kuma ci 'ya'yansa.
30 Sau ɗaya kuma ragowar masarautar Yahuda
za tă yi saiwoyi a ƙasa ta kuma ba da 'ya'ya a bisa.
31 Gama daga Urushalima za a sami ragowa,
daga Dutsen Sihiyona kuma za a sami waɗanda suka tsira.
Himmar UBANGIJI Maɗaukaki za tă cika wannan.

32 "Saboda haka ga abin da UBANGIJI ya ce game da sarkin Assuriya,
"Ba zai shiga birnin nan ba
ko yă harba kibiya a nan.
Ba zai kusace ta da garkuwa
ko yă yi mata zoben yaƙi ba.
33 Ta hanyar da ya zo ne zai koma;
ba zai shiga birnin nan ba, in ji UBANGIJI.
34 Zan kāre birnin nan in cece ta,
saboda kaina da kuma bawana Dawuda."

*(Ishaya 37.36-38)*

35 A daren nan mala'ikan UBANGIJI ya fita ya kashe dakaru dubu ɗari da tamanin
da biyu a sansanin Assuriyawa. Da mutane suka farka da safe, sai ga gawawwaki
ko'ina. 36 Saboda haka Sennakerib sarkin Assuriya ya tā da sansanin ya kuma janye.
Ya koma Ninebe ya zauna a can.

37 Wata rana yayinda yake sujada a haikalin Nisrok, allahnsa, sai ʼyaʼyansa maza,
Adrammelek da Sharezer suka kashe shi da takobi, suka gudu zuwa ƙasar Ararat.
Sai Esar-Haddon ɗansa ya gāje shi.

# 20

### *Ciwon Hezekiya*
### *(2 Tarihi 32.24-26; Ishaya 38.1-8,21,22)*

1 A kwanakin nan sai Hezekiya ya kamu da rashin lafiya har ya kusa mutuwa. Sai
annabi Ishaya ɗan Amoz ya zo wurinsa ya ce, "Ga abin da UBANGIJI ya ce, ka kintsa
gidanka domin za ka mutu, ba za ka warke ba."

2 Hezekiya ya juya fuskarsa wajen bango ya yi adduʼa ga UBANGIJI ya ce, 3 "Ya
UBANGIJI, ka tuna yadda na yi tafiya a gabanka da aminci da zuciya ɗaya, na kuma
aikata abin da yake daidai a gabanka." Sai Hezekiya ya yi kuka mai zafi.

4 Kafin Ishaya yă bar tsakiyar filin gida, sai maganar UBANGIJI ta zo masa cewa,
5 "Ka koma ka ce wa Hezekiya, shugaban mutanena, 'Ga abin da UBANGIJI Allah na
mahaifinka Dawuda ya ce, na ji adduʼarka na kuma ga hawayenka; zan warkar da
kai. A rana ta uku daga yau za ka haura zuwa haikalin UBANGIJI. 6 Zan ƙara maka
shekara goma sha biyar. Zan kuma cece ka daga hannun sarkin Assuriya. Zan kāre
birnin nan saboda kaina da kuma bawana Dawuda.' "
7 Sai Ishaya ya ce, "A kwaɓa ɓaure." Sai aka yi haka, aka shafa wa marurun, ya
kuma warke.
8 Hezekiya ya tambayi Ishaya, "Wace alama ce za tă nuna cewa UBANGIJI zai warkar
da ni, kuma cewa in tafi haikalin UBANGIJI kwana uku daga yanzu?"

9 Sai Ishaya ya ce, "Ga alamar UBANGIJI zuwa gare ka da za tă nuna cewa UBANGIJI
zai cika alkawarinsa. Kana so inuwa tă yi gaba da taki goma, ko tă koma baya da
taki goma?"

10 "Ai, abu mai sauƙi ne inuwa tă yi gaba da taki goma." In ji Hezekiya, "Gwamma
dai tă koma baya da taki goma."

11 Sai annabi Ishaya ya roƙi UBANGIJI, UBANGIJI kuwa ya sa inuwa ta koma baya da
taki goma bisa ga magwajin rana wanda Sarki Ahaz ya gina.

### *Jakadu daga Babilon*
### *(Ishaya 39.1-8)*

12 A wannan lokaci, Merodak-Baladan ɗan Baladan sarkin Babilon ya aika wa
Hezekiya wasiƙu tare da kyauta, domin ya sami labarin rashin lafiyar Hezekiya.
13 Hezekiya ya karɓi jakadun, ya nuna musu dukan abin da yake a ɗakunan ajiyarsa,
azurfa, zinariya, kayan ƙanshi da mai, wurin ajiye makamansa da kuma dukan abin
da aka samu a ɗakin ajiyarsa. Babu wani abu a fadansa ko a dukan mulkinsa da
Hezekiya bai nuna musu ba.

14 Sai annabi Ishaya ya tafi wurin Sarki Hezekiya ya tambaye shi ya ce, "Me
mutanen nan suka ce, kuma daga ina suka fito?"

Sai Hezekiya ya ce, "Daga ƙasa mai nisa. Daga Babilon."

15 Annabin ya yi tambaya, "Me suka gani a fadanka?"

Hezekiya ya ce, "Ba abin da yake a maʼajina da ban nuna musu ba."

16 Sai Ishaya ya ce wa Hezekiya, "Ka ji kalmar UBANGIJI. 17 Lokaci yana zuwa da
za a kwashe kome a fadanka da kuma dukan abubuwan da kakanninka suka tara
har yă zuwa yau, a kai su Babilon. Ba abin da za a rage, in ji UBANGIJI. 18 Za a kuma
kwashe waɗansu daga cikin zuriyarka, na jiki da jininka waɗanda za a haifa maka,
su zama bābānni a fadan sarkin Babilon."

[19] Hezekiya ya ce, "Maganar Ubangiji da ka faɗa ta yi kyau." Gama ya yi tunani
cewa, "Ai, ba ni da damuwa, tun da yake za a yi zaman lafiya da salama a kwanakina."

*(2 Tarihi 32.32,33)*

[20] Game da sauran ayyukan mulkin Hezekiya, dukan nasarorinsa da yadda ya yi
tafki da kuma bututun ruwa inda ya kawo ruwa cikin birni, duk a rubuce suke a cikin
littafin tarihin sarakunan Yahuda. [21] Hezekiya ya huta tare da kakanninsa. Manasse
ɗansa kuma ya gāje shi.

# 21

*Manasse sarkin Yahuda*
*(2 Tarihi 33.1-20)*

[1] Manasse yana da shekara goma sha biyu sa'ad da ya zama sarki, ya yi mulki
shekara hamsin da biyar a Urushalima. Sunan mahaifiyarsa Hefziba. [2] Ya aikata
mugunta a gaban Ubangiji, ya bi munanan al'adun al'umman da Ubangiji ya kora a
gaban Isra'ilawa. [3] Ya sāke gina masujadan da mahaifinsa Hezekiya ya rurrushe. Ya
kuma gina wa Ba'al bagadai. Ya kafa ginshiƙin Ashera kamar yadda Ahab sarkin
Isra'ila ya yi. Ya durƙusa wa dukan rundunan taurari ya yi musu sujada. [4] Ya
gina bagadai a haikalin Ubangiji, wurin da Ubangiji ya ce, "A Urushalima ne zan
sa Sunana." [5] Cikin filaye biyu na haikalin Ubangiji kuwa, ya gina bagadai na dukan
rundunan taurari. [6] Ya miƙa ɗansa hadaya ta ƙonawa, ya yi sihiri da tsubu, ya
tuntuɓi masu duba da masu ruhohi. Ya aikata mugunta ƙwarai a gaban Ubangiji, ya
sa Ubangiji ya yi fushi.

[7] Ya ɗauki siffar ginshiƙin Asherar da ya yi, ya sa a haikalin da Ubangiji ya ce wa
Dawuda da ɗansa Solomon, "A cikin wannan haikali, da kuma cikin Urushalima inda
na zaɓa daga kabilan Isra'ila, zan sa Sunana har abada. [8] Ba zan ƙara sa Isra'ilawa su
fita daga ƙasar da na ba kakanninsu ba, idan dai za su kula su aikata dukan abin da
na umarce su, su kuma kiyaye dukan dokokin da na ba wa bawana Musa yǎ umarce
su." [9] Amma mutanen ba su kasa kunne ba. Manasse ya ɓad da su, har suka yi
muguntar da ta fi ta al'umman da Ubangiji ya hallaka a gaban Isra'ilawa.

[10] Ubangiji ya yi magana ta bakin bayinsa annabawa, [11] "Manasse, sarkin Yahuda
ya aikata waɗannan ƙazantattun zunubai. Ya aikata mugunta fiye da ta Amoriyawan
da suka riga shi, ya kuma sa Yahuda ta bauɗe ta wurin yin zunubi saboda gumakansa.
[12] Saboda haka ga abin da Ubangiji, Allah na Isra'ila ya ce, zan jawo wa Urushalima
da kuma Yahuda masifar da duk kunnen da ya ji, sai ya kusa suma. [13] Zan auna
Urushalima da ma'aunin da na yi amfani da shi a kan Samariya, zan kuma yi amfani
da magwajin da na yi amfani da shi a kan gidan Ahab. Zan shafe Urushalima yadda
mutum yake wanke kwano yǎ kife. [14] Zan rabu da ragowar gādona, in kuma miƙa su
ga maƙiyansu. Abokan gābansu za su washe suka kuma kwashi ganima daga gare
su, [15] domin sun aikata mugunta a idanuna, suka kuma tsokane ni tun daga ranar da
kakanninsu suka fito daga Masar, har yǎ zuwa yau."

[16] Ban da haka ma, Manasse ya zub da jinin marasa laifi har ya cika Urushalima
daga wannan ɓangare zuwa wancan, ban da zunubin da ya sa Yahuda ta aikata, ta
haka suka yi mugunta a gaban Ubangiji.

[17] Game da sauran ayyukan mulkin Manasse, da duk abin da ya yi, har da zunubin
da ya aikata, duk a rubuce suke a cikin littafin tarihin sarakunan Yahuda. [18] Manasse
ya huta tare da kakanninsa, aka kuma binne shi a lambun fadansa, lambun Uzza. Sai
Amon ɗansa ya gāje shi.

*Amon sarkin Yahuda*
*(2 Tarihi 33.21-25)*

[19] Amon yana da shekara ashirin da biyu sa'ad da ya zama sarki, ya yi mulki
shekara biyu a Urushalima. Sunan mahaifiyarsa Meshullemet 'yar Haruz; ita
mutuniyar Yotba ce. [20] Ya aikata mugunta a gaban UBANGIJI, yadda Manasse
mahaifinsa ya yi. [21] Ya bi duk gurbin mahaifinsa a kome, ya yi sujada ga gumakan
da mahaifinsa ya yi wa, ya kuma durƙusa musu. [22] Ya rabu da UBANGIJI Allah na
kakanninsa, bai kuwa yi tafiya a hanyar UBANGIJI ba.

[23] Fadawan Amon suka ƙulla maƙarƙashiya suka kashe shi a cikin fadarsa. [24] Sai
mutanen ƙasar suka kashe duk waɗanda suka ƙulla wa Sarki Amon maƙarƙashiya,
sa'an nan suka naɗa ɗansa sarki a maimakonsa.
[25] Game da sauran ayyukan mulkin Amon, da abubuwan da ya aikata, duk a rubuce
suke a cikin littafin tarihin sarakunan Yahuda. [26] Aka binne shi a kabarinsa a lambun
Uzza. Yosiya ɗansa kuma ya gāje shi.

# 22

*An sami Littafin Doka*
*(2 Tarihi 34.1,2)*

[1] Yosiya yana da shekara takwas sa'ad da ya zama sarki, ya kuma yi mulki shekara
talatin da ɗaya a Urushalima. Sunan mahaifiyarsa Yedida 'yar Adahiya; mutuniyar
Bozkat. [2] Ya aikata abin da yake daidai a gaban UBANGIJI ya kuma bi dukan gurbin
kakansa Dawuda, bai bauɗe hagu ko dama ba.

*(2 Tarihi 34.8-28)*

[3] A shekara ta goma sha takwas ta mulkinsa, Sarki Yosiya ya aiki Shafan ɗan
Azaliya, ɗan Meshullam, magatakarda, zuwa haikalin UBANGIJI. Ya ce, [4] "Ka haura
zuwa wurin Hilkiya babban firist ka sa yǎ shirya kuɗin da aka kawo a haikalin
UBANGIJI, wanda masu tsaron ƙofa suka tara daga mutane. [5] Ka sa su danƙa su
a hannun waɗanda aka zaɓa don biyan ma'aikatan da suka yi gyara a haikalin
UBANGIJI, [6] wato, kafintoci, da magina, da masu tsara gini. Ka kuma sa su sayi katakai
da sassaƙaƙƙun duwatsu don a gyara haikalin. [7] Amma ba sa bukata su ba da bayanin
kuɗin da aka danƙa musu domin suna aikinsu da aminci."
[8] Hilkiya babban firist ya ce wa Shafan magatakarda, "Na sami Littafin Doka a
haikalin UBANGIJI." Sai ya ba wa Shafan, shi kuma ya karanta. [9] Sa'an nan Shafan
ya koma wurin sarki ya ce masa, "Hafsoshinka sun kwashe kuɗin da suke a haikalin
UBANGIJI, suka ba wa masu aiki da masu lura da haikalin." [10] Sa'an nan Shafan
magatakarda ya ce wa sarki, "Hilkiya firist ya ba ni wani littafi." Sai Shafan ya
karanta shi a gaban sarki.

[11] Da sarki ya ji kalmomin Littafin Doka, sai ya kece tufafinsa. [12] Ya ba da waɗannan
umarnai ga Hilkiya firist, da Ahikam ɗan Shafan, da Akbor ɗan Mikahiya, da Shafan
magatakarda, da kuma Asahiya mai hidimar sarki, ya ce, [13] "Ku je, ku nemi nufin
UBANGIJI saboda ni da saboda jama'a da kuma saboda dukan Yahuda game da abin
da wannan littafi da aka samo ya ƙunsa. Fushin UBANGIJI mai girma ne a kanmu
domin kakanninmu ba su kiyaye kalmomin littafin nan ba; ba su aikata bisa ga abin
da yake a rubuce game da mu ba."

[14] Sai Hilkiya firist, da Ahikam, Akbor, da Shafan, da kuma Asahiya suka je don
su yi magana da annabiya Hulda, matan Shallum ɗan Tikba, ɗan Harhas, mai ajiyar
tufafi. Tana zama a Urushalima, a Yanki na Biyu.

[15] Sai ta ce musu, "Ga abin da UBANGIJI, Allah na Isra'ila ya ce, ku faɗa wa mutumin
da ya aike ku wurina, [16] 'Ga abin da UBANGIJI ya ce, zan kawo masifa wa wannan wuri
da kuma wa kan mutanen wurin, bisa ga dukan abubuwan da suke a rubuce a cikin
littafin da sarkin Yahuda ya karanta. [17] Domin sun yashe ni suka ƙona turare wa

waɗansu alloli, suka tozarta ni da dukan gumakan da hannuwansu suka sassaƙa,*
fushina zai yi ƙuna a kan wannan wuri, ba kuwa zai huce ba.' [18] Ku faɗa wa sarkin
Yahuda, wanda ya aike ku ku nemi nufin Ubangiji, 'Ga abin da Ubangiji, Allah na
Isra'ila yana cewa game da kalmomin da ka ji. [19] Domin zuciyarka mai tuba ce, ka
kuma ƙasƙantar da kanka a gaban Ubangiji sa'ad da ka ji abin da na faɗa game da
wannan wuri da mutanen wurin, cewa za su zama la'antattu da kuma kango, domin
kuma ka kece tufafinka, ka kuma yi kuka a gabana, na ji ka, in ji Ubangiji. [20] Saboda
haka zan haɗa ka da kakanninka, za a kuma binne ka cikin salama. Idanunka kuma
ba za su ga dukan wannan masifan da zan jawo wa wurin nan ba.' "

Sai suka kai wa sarki abin da ta faɗa.

# 23

*Yosiya ya sabunta alkawari*
*(2 Tarihi 34.29-33)*

[1] Sai sarki ya kira dukan dattawan Yahuda da Urushalima. [2] Sai ya haura zuwa
cikin haikalin Ubangiji tare da mutanen Yahuda, da na Urushalima, da firistoci, da
annabawa, dukan mutane, manya da ƙanana. Ya karanta musu duk kalmomin
Littafin Alkawari, wanda aka samu a haikalin Ubangiji. [3] Sarki ya tsaya dab da
ginshiƙi ya kuma sabunta alkawarin a gaban Ubangiji, ya ce zai bi Ubangiji, yă kiyaye
dokokinsa, da ƙa'idodinsa, da farillansa, da dukan zuciyarsa da dukan ransa, ta haka
ya tabbatar da kalmomin alkawarin da yake a rubuce a cikin littafin nan. Sa'an nan
dukan mutane ma suka yi alkawari yin haka.

*(2 Tarihi 34.3-7)*

[4] Sai Yosiya ya umarci Hilkiya babban firist, tare da firistocin da suke taimakonsa,
da masu tsaron ƙofa su kawar da dukan abubuwan da aka yi domin Ba'al, da domin
Ashera, da kuma domin dukan rundunar taurari, daga haikalin Ubangiji. Ya ƙone
su a bayan Urushalima a filayen Kwarin Kidron, ya kwashe tokan zuwa Betel. [5] Ya
kawar da firistocin gumakan da sarakunan Yahuda suka naɗa don su ƙona turare
a masujadan kan tuddai na garuruwan Yahuda, da kuma waɗanda suke kewaye da
Urushalima, masu ƙona turare wa Ba'al, rana da wata, ga rukunin taurari, da kuma
ga dukan rundunan taurari. [6] Ya ɗauke ginshiƙin Ashera daga haikalin Ubangiji zuwa
Kwarin Kidron can bayan Urushalima, ya ƙone shi a can. Ya niƙa shi sai da ya zama
toka, sai ya watsar da ƙurar a filin kabarin talakawa. [7] Ya kuma rurrushe mazaunan
karuwai mazan haikali waɗanda suke a haikalin Ubangiji, da kuma inda mata suke
yi wa Ashera saƙa.

[8] Yosiya ya kawo dukan firistoci daga garuruwan Yahuda, ya kuma lalatar da
masujadan kan tuddai daga Geba har zuwa Beyersheba, inda firistoci suke ƙona
turare. Ya rurrushe matsafai a ƙofofi shigan gari na mashigi zuwa Kofar Yoshuwa,
gwamnan birnin, wanda yake a hagu da ƙofar birnin. [9] Ko da yake firistocin
masujadan kan tuddai ba su yi hidima a bagaden Ubangiji a Urushalima ba, sun
ci burodi marar yisti tare da sauran firistoci.

[10] Ya lalatar da Tofet, wanda yake a Kwarin Ben Hinnom, don kada kowa yă iya
yin amfani da wurin don yă miƙa hadayar ɗansa, ko 'yarsa a* wuta ga Molek. [11] Ya
kawar da dawakan nan da sarakunan Yahuda suka keɓe wa gumakan nan na rana
daga mashigin haikalin Ubangiji. Waɗannan dawakan suna kusa da ɗakin Natan
Melek, ɗaya daga cikin dattawan sarki. Yosiya ya kuma ƙone kekunan yaƙi a yin
sujada ga gumakan nan rana.

* **22:17** Ko kuwa ta wurin dukan abubuwan da suka aikata ratsa

* **23:10** Ko kuwa don yă sa ɗansa ko 'yarsa ta

12 Ya rushe bagadan da sarakunan Yahuda suka kafa a kan ɗakin sama kusa da ɗakin sama na Ahaz, da kuma bagadai biyu da Manasse ya gina a filaye biyu na haikalin UBANGIJI. Ya kawar da su daga can, ya farfashe su, ya zubar da tarkacen a
Kwarin Kidron. 13 Sarkin kuma ya lalatar da masujadan kan tuddan da suke gabas da Urushalima, kudu da Tudun Hallaka, waɗanda Solomon sarkin Isra'ila ya gina don Ashtarot, ƙazantacciyar alliyar Sidoniyawa, da Kemosh ƙazantaccen allah na Mowab, da kuma Molek† allahn banƙyama na mutanen Ammon. 14 Yosiya ya farfashe
keɓaɓɓun duwatsu, ya rurrushe ginshiƙan Asheransu, ya baza ƙasusuwan mutane a can.

15 Har ma da bagaden Betel, masujadan kan tudun da Yerobowam ɗan Nebat ya yi, wanda ya sa Isra'ila suka yi zunubi. Wannan bagade da masujadan kan tudun ma ya kawar, ya ƙone masujadan kan tudun, ya niƙa su, ya kuma ƙone ginshiƙin Ashera.
16 Da Yosiya ya dubi kewaye da shi, ya ga kaburburan da suke can a gefen tudu, sai ya sa aka kwaso ƙasusuwan da suke cikinsu aka ƙone a kan bagade don yă lalatar da shi bisa ga maganar UBANGIJI ta bakin mutumin Allah, wanda ya yi annabcin waɗannan abubuwa.

17 Sarkin ya yi tambaya, ya ce, "Wane kabari ke nan nake gani?"

Mutanen birnin suka ce, "Ai, kabarin annabin Allah ne wanda ya fito daga Yahuda, shi ne ya yi annabcin waɗannan abubuwan da ka aikata gāba da bagaden Betel."

18 Sai ya ce, "Ku rabu da shi, kada wani yă dami ƙasusuwansa." Saboda haka suka bar kasusuwansa, da na annabin da ya fito Samariya.

19 Kamar yadda ya yi a Betel, Yosiya ya kawar da dukan ɗakunan gumaka a kan tuddan da sarakunan Isra'ila suka gina a garuruwan Samariya, waɗanda suka tozarta
UBANGIJI. 20 Yosiya ya yayyanka dukan firistoci na waɗannan masujadan kan tuddai, ya kuma ƙone ƙasusuwan mutane a kansu. Sa'an nan ya koma Urushalima.

*(2 Tarihi 35.1-19)*

21 Sarkin ya ba da umarnin nan ga dukan mutane, cewa, "Ku yi Bikin Ketarewa ga UBANGIJI Allahnku, yadda aka rubuta a Littafin Alkawari." 22 Ba a taɓa yin irin Bikin Ketarewa haka ba, tun zamanin da masu shari'a suke aiki a matsayin sarakuna, ko a kwanakin sarakunan Isra'ila, ko na Yahuda. 23 Amma a shekara ta goma sha takwas ta mulkin sarki Yosiya, aka yi Bikin Ketarewan nan ga UBANGIJI a Urushalima.

24 Ban da haka, Yosiya ya kawar da masu duba, da masu maita, da allolin gidaje, da gumaka, da duk wani abin banƙyaman da ya gani a Yahuda da Urushalima. Ya yi wannan domin yă cika wa'adodin shari'a yadda suke a littafin da Hilkiya firist ya samu a haikalin UBANGIJI. 25 Babu wani sarki kafin Yosiya, ko kuma a bayansa, wanda ya juya ga UBANGIJI da dukan zuciyarsa, da dukan ransa, da dukan ƙarfinsa bisa ga shari'ar Musa, kamar yadda ya yi.

26 Duk da haka, UBANGIJI bai huce daga zafin fushinsa wanda ya ƙuna game da Yahuda saboda abin da Manasse ya aikata don yă tozarta shi ba. 27 Saboda haka
UBANGIJI ya ce, "Zan shafe Yahuda ma kamar yadda na shafe Isra'ila, daga gabana, zan ƙi Urushalima birnin da na zaɓa, da wannan haikali wanda na ce, 'A can Sunana zai kasance.' "‡

*(2 Tarihi 35.20–36.1)*

28 Game da sauran ayyukan mulkin Yosiya, da duk abin da ya yi, duk a rubuce suke a cikin littafin tarihin sarakunan Yahuda.

29 Yayinda Yosiya yake sarki, Fir'auna Neko, sarkin Masar ya haura zuwa Kogin Yuferites don yă taimaki sarkin Assuriya da yaƙi. Sarki Yosiya kuwa ya yi ƙoƙari ya hana shi wucewa, sa'ad da Fir'auna Neko ya gan shi, sai ya kashe shi a filin yaƙi a
Megiddo. 30 Bayin Yosiya suka ɗauko gawarsa daga Megiddo suka kai Urushalima,

† **23:13** Da Ibraniyanci Milkom ‡ **23:27** 1Sar 8.29.

suka binne shi a kabarinsa. Sai mutanen ƙasar suka ɗauki Yehoyahaz ɗan Yosiya suka naɗa shi sarki a madadin mahaifinsa.

### *Yehoyahaz sarkin Yahuda (2 Tarihi 36.2-4)*

31 Yehoyahaz yana da shekara ashirin da uku sa'ad da ya zama sarki. Ya yi mulki
na wata uku a Urushalima. Sunan mahaifiyarsa Hamutal 'yar Irmiya; mutuniyar
Libna. 32 Ya aikata mugunta a gaban UBANGIJI, yadda kakanninsa suka yi. 33 Fir'auna
Neko ya sa shi a sarƙa a Ribla a ƙasar Hamat§ don kada yǎ yi mulki a Urushalima,
sa'an nan ya sa wa Yahuda harajin talenti ɗari na azurfa, da talenti ɗaya na zinariya.
34 Fir'auna Neko ya naɗa Eliyakim ɗan Yosiya sarki a maimakon mahaifinsa, ya kuma
canja masa suna zuwa Yehohiyakim. Ya ɗauki Yehoyahaz ya kai Masar, a can ya mutu.
35 Yehohiyakim ya riƙa biyan Fir'auna Neko azurfa da zinariyar da ya umarta. Don
yǎ yi haka sai ya riƙa karɓar azurfa da zinariya daga mutanen ƙasar, kowa bisa ga
ƙarfinsa.

### *Yehohiyakim sarkin Yahuda (2 Tarihi 36.5-8)*

36 Yehohiyakim yana da shekara ashirin da biyar sa'ad da ya zama sarki, ya kuma
yi mulki shekara goma sha ɗaya a Urushalima. Sunan mahaifiyarsa Zebuda 'yar
Fedahiya, mutuniyar Ruma. 37 Ya kuma aika mugunta a gaban UBANGIJI yadda
kakanninsa suka yi.

## 24

1 A zamani Yehohiyakim, Nebukadnezzar sarkin Babilon ya kawo wa ƙasar
farmaki, Yehohiyakim dai ya zama abokin tarayyarsa na tsawon shekara uku. Daga
baya kuma sai ya canja ra'ayi ya yi wa Nebukadnezzar tawaye. 2 UBANGIJI ya aiki
maharan Babiloniyawa,* da na Arameyawa, da na Mowabawa, da na Ammonawa.
Ya aike su su hallaka Yahuda bisa ga maganar UBANGIJI wadda ya furta ta bakin
bayinsa annabawa. 3 Ba shakka waɗannan abubuwa sun faru da Yahuda bisa ga
umarnin UBANGIJI domin yǎ kawar da su daga gabansa saboda zunuban Manasse
da dukan abin da ya yi, 4 haɗe da zub da jinin marasa laifi. Gama ya ƙazantar da
Urushalima da jinin marasa laifi. UBANGIJI kuwa bai yi niyyar yafewa ba.
5 Game da sauran ayyukan mulkin Yehohiyakim da abubuwan da ya aikata, duk
a rubuce suke a cikin littafin tarihin sarakunan Yahuda. 6 Yehohiyakim ya huta da
kakanninsa. Yehohiyacin ɗansa ya gāje shi.
7 Sarkin Masar bai sāke fita daga ƙasarsa don yaƙi ba domin sarkin Babilon ya
mamaye yankin, daga Rafin Masar har zuwa Kogin Yuferites.

### *Yehohiyacin sarkin Yahuda (2 Tarihi 36.9,10)*

8 Yehohiyacin yana da shekara goma sha takwas da ya zama sarki, ya kuma yi
mulki wata uku a Urushalima. Sunan mahaifiyarsa Nehushta 'yar Elnatan, mutuniyar
Urushalima. 9 Ya aikata mugunta a gaban UBANGIJI yadda mahaifinsa ya yi.
10 A wannan lokaci, hafsoshin Nebukadnezzar sarkin Babilon suka kawo wa
Urushalima yaƙi, suka kuma kewaye ta. 11 Nebukadnezzar na Babilon da kansa kuwa
ya zo birnin yayinda hafsoshinsa suka kewaye ta. 12 Yehohiyacin sarkin Yahuda, da
mahaifiyarsa, da masu yi masa hidima, da hakimansa, da kuma fadawansa duk suka
miƙa kansu ga Nebukadnezzar.

---

§ **23:33** Da Ibraniyanci; Seftuwajin (dubi kuma 2Tar 36.3) Neko a Ribla in Hamat ya cire shi
* **24:2** Ko kuwa Kaldiyawa

A shekara ta takwas ta mulkin sarkin Babilon, sarkin Babilon ya mai da Yehohiyacin
ɗan kurkuku. 13 Yadda UBANGIJI ya faɗa, Nebukadnezzar ya kwashe dukan dukiyar
haikalin UBANGIJI, da ta fadan sarki, ya kuma kwashe dukan kayan zinariyar da
Solomon sarkin Isra'ila ya ƙera domin haikalin UBANGIJI. 14 Ya kwashi dukan
mutanen Urushalima zuwa bauta, ya kwashi dukan fadawa, da mayaƙa, da masu
sana'a, da maƙera, yawansu ya kai dubu goma. Ba wanda ya ragu, sai matalautan
ƙasar.
15 Nebukadnezzar ya ɗauki Yehohiyacin ya kai bauta a Babilon. Ya kuma kwashe
mahaifiyar sarki, da matansa, da fadawansa, da manyan mutanen ƙasar daga
Urushalima ya kai Babilon. 16 Sarkin Babilon kuma ya kwashe dukan mayaƙa dubu
bakwai, ƙarfafu, shiryayyu don yaƙi, da masu sana'a, da maƙera dubu ɗaya, ya kai
Babilon. 17 Sarkin Babilon ya sa Mattaniya, ɗan'uwan mahaifin Yehohiyacin, ya zama
sarki a madadinsa, ya canja masa suna zuwa Zedekiya.

*Zedekiya sarkin Yahuda*
*(2 Tarihi 36.11-16; Irmiya 52.1-3)*

18 Zedekiya yana da shekara ashirin da ɗaya da ya zama sarki, ya kuma yi mulki
shekara goma sha ɗaya a Urushalima. Sunan mahaifiyarsa Hamutal 'yar Irmiya;
mutuniyar Libna. 19 Ya aikata mugunta a gaban UBANGIJI yadda Yehohiyakim ya yi.
20 Saboda fushin UBANGIJI ne dukan waɗannan abubuwa suka faru da Urushalima,
da kuma Yahuda, a ƙarshe kuma ya kawar da su daga fuskarsa.

*Fāɗuwar Urushalima*

To, sai Zedekiya ya yi wa sarkin Babilon tawaye.

## 25

*(2 Tarihi 36.17-21; Irmiya 52.3-30)*

1 A rana ta goma ga wata na goma, a shekara ta tara ta mulkin Zedekiya ne
Nebukadnezzar sarkin Babilon tare da dukan rundunan yaƙinsa, ya tasam wa
Urushalima. Ya yi sansani a bayan birnin, ya kewaye ta da shirin yaƙi. 2 Haka birnin
ta kasance a kewaye har shekara ta goma sha ɗaya ta mulkin Zedekiya.
3 A rana ta tara ta watan huɗu, lokacin da yunwa ta yi tsanani a birnin, babu
kuma abinci domin mutane su ci. 4 Sai aka huda katanga sa'an nan dukan sojoji
suka tsere da dare a ƙofa tsakanin katanga biyu da suke kusa da lambun sarki, ko da
yake Babiloniyawa sun kewaye birnin. Suka tsere suka nufi Araba. 5 Amma sojojin
Babiloniyawa suka bi sarki, suka cin masa a filayen Yeriko. Dukan sojojinsa kuwa
suka rabu da shi suka watse.
6 Aka kama shi, aka kai shi gaban sarkin Babilon a Ribla, inda aka yanke masa
hukunci. 7 Suka kashe 'ya'yan Zedekiya a gabansa, sa'an nan aka ƙwaƙule idanunsa.
Suka daure shi da sarƙar tagulla, suka kai shi Babilon.
8 A rana ta bakwai na watan biyar, wadda ta zama shekara ta goma sha tara ta
mulkin Sarki Nebukadnezzar na Babilon, Nebuzaradan, babban hafsan matsaran
sarki, kuma bafadan sarkin Babilon, ya zo Urushalima 9 Ya cinna wa haikalin UBANGIJI
wuta, da fadan sarki, da kuma dukan gidajen Urushalima. Ya kuma ƙone duk wani
gini mai muhimmanci. 10 Dukan mayaƙan Babilon a ƙarƙashin umarnin babban
hafsan matsaran sarki, suka rushe katangar Urushalima. 11 Nebuzaradan babban
hafsan matsaran, ya kwashi waɗanda suka rage a cikin birnin, tare da sauran jama'a,
da waɗanda suka miƙa kansu ga sarkin Babilon, ya kai su bauta. 12 Amma hafsan ya
bar waɗansu daga cikin mafiya talauci na ƙasar don su yi aiki a lambunan inabi da
kuma gonaki.
13 Babiloniyawan kuma suka sassare ginshiƙan tagulla, da wuraren zama da za
a iya matsar da su, da ƙaton kwano mai suna Teku na tagulla da yake a haikalin

UBANGIJI, suka kwashe tagullan zuwa Babilon. 14 Suka ɗauke tukwane, da manyan
cokula, da acibalbal, da kwanoni, da dai dukan kayan da aka yi da tagulla don hidima
a haikalin UBANGIJI. 15 Babban hafsan matsaran sarkin ya kwashe har da kwanoni
na kwashe garwashin wuta da sauran kwanoni, dukansu kuwa ƙeran zinariya ko
azurfa tsatsa ne.
16 Tagullar ginshiƙai biyun nan, da ta ƙaton kwanon da ake ce da shi Teku, da
ta dukan amalanke masu riƙe ruwa waɗanda Sarki Solomon ya yi domin haikalin
UBANGIJI, sun fi gaba a auna su. 17 Tsawon kowane ginshiƙi, ƙafa ashirin da bakwai
ne. Hulunan tagullan da suke ƙwalƙwalin kowane ginshiƙi kuma yana da tsawon
ƙafa huɗu da rabi. Kuma aka yi masa ado da saƙa da 'ya'yan itace kewaye da shi.
Bayan ginshiƙin ma haka yake.
18 Babban hafsan ya kwashi Serahiya babban firist, da Zefaniya na biye da shi a
girma, da matsara ƙofofi uku. 19 Daga cikin waɗanda suka rage a birnin, ya ɗauki
hafsa mai kula da dakaru, da kuma mashawartan sarki guda biyar. Ya kuma tafi
da magatakarda wanda yake babban jami'in soja mai ɗaukan dukan jama'an ƙasar,
tare da mutanensa guda sittin waɗanda aka samu a birnin. 20 Nebuzaradan, babban
hafsan, ya kwashe su duka ya kawo su wurin sarkin Babilon a Ribla. 21 A can Ribla,
a ƙasar Hamat, sarkin Babilon ya sa aka kashe su. Haka Yahuda ta tafi bauta daga
ƙasarta.

*(Irmiya 40.7-9; 41.1-3)*

22 Nebukadnezzar sarkin Babilon ya zaɓi Gedaliya ɗan Ahikam, ɗan Shafan yǎ
zama shugaban sauran mutanen da suka rage a Yahuda. 23 Sa'ad da dukan hafsoshin
soja tare da mutanensu suka ji cewa sarkin Babilon ya naɗa Gedaliya a matsayin
gwamna, sai suka zo wurin Gedaliya a Mizfa. Mutanen da suka zo su ne, Ishmayel ɗan
Netaniya, Yohanan ɗan Kareya, Serahiya ɗan Tanhumet mutumin Netofa, Ya'azaniya
ɗan mutumin Ma'aka, tare da mutanensu. 24 Gedaliya ya tabbatar musu da rantsuwa
cewa, "Kada ku ji tsoron jama'ar Babiloniyawa, muddin kun zauna lafiya, kun kuma
bauta wa sarkin Babilon, kome zai yi muku kyau."
25 Amma a wata na bakwai, sai Ishmayel, ɗan Netaniya, ɗan Elishama, wanda yake
daga gidan sarauta, ya zo tare da mutane goma, suka kashe Gedaliya duk da mutanen
Yahuda, da na Babilon da suke tare da shi na Mizfa. 26 Ganin haka sai dukan mutane,
babba da ƙarami, tare da shugabannin sojoji, suka tashi suka gudu zuwa ƙasar Masar,
gama suna tsoron mutanen Babilon.

### *An saki Yehohiyacin*
*(Irmiya 52.31-34)*

27 A shekara ta talatin da bakwai ta bautar Yehohiyacin sarkin Yahuda, a shekaran
da Ewil-Merodak* ya ci sarautan Babilon, sai ya saki Yehohiyacin daga jaru, ya sake
shi a rana ashirin da bakwai ga watan goma sha biyu. 28 Ya yi wa Yehohiyacin
maganar alheri, ya kuma ɗaukaka shi sama da sauran sarakunan da suke tare da
shi a Babilon. 29 Don haka Yehohiyacin ya tuɓe kayan fursuna. Kowace rana kuwa
yakan ci abinci a teburin sarki har iyakar ransa. 30 Sarki kuma ya yanka masa kuɗin
da za a dinga ba shi, kowace rana muddin ransa.

* **25:27** Da ake kuma kira Amel-Marduk

# 1 Tarihi

## *Rubutaccen tarihi daga Adamu zuwa Ibrahim*

### *Zuwa ʼYaʼyan Nuhu Maza*
### *(Farawa 5.1-32; 10.1-32; 11.10-32)*

1 Adamu, Set, Enosh,
2 Kenan, Mahalalel, Yared,
3 Enok, Metusela, Lamek, Nuhu.

4 ʼYaʼyan Nuhu maza su ne,* Shem, Ham da Yafet.

### *Mutanen Yafet*

5 ʼYaʼyan† Yafet maza su ne,
Gomer, Magog, Madai, Yaban, Tubal, Meshek da Tiras.
6 ʼYaʼyan Gomer maza su ne,
Ashkenaz, Rifat‡ da Togarma.
7 ʼYaʼyan Yaban maza su ne,
Elisha, Tarshish, Kittim da Rodanim.

### *Mutanen Ham*

8 ʼYaʼyan Ham maza su ne,
Kush, Masar§ Fut da Kanʼana.
9 ʼYaʼyan Kush maza su ne,
Seba, Hawila, Sabta, Raʼama da Sabteka.
ʼYaʼyan Raʼama maza su ne,
Sheba da Dedan
10 Kush shi ne mahaifin*
Nimrod, wanda ya yi girma ya zama babban jarumi a duniya.
11 Masar shi ne mahaifin
Ludiyawa, Anamawa, Lehabiyawa, Neftuhawa,
12 Fatrusawa, Kasluhiyawa (daga waɗanda Filistiyawa suka fito) da Kaftorawa.
13 Kanʼana shi ne mahaifin
Sidon ɗan farinsa, da Hittiyawa,
14 Yebusiyawa, Amoriyawa, Girgashiyawa
15 Hiwiyawa, Arkiyawa, Siniyawa,
16 Arbadiyawa, Zemarawa da Hamawa.

### *Semiyawa*

17 ʼYaʼyan Shem maza su ne,
Elam, Asshur, Arfakshad, Lud da Aram.
ʼYaʼyan Aram maza su ne,
Uz, Hul, Geter da Meshek.
18 Arfakshad shi ne mahaifin Shela,
Shela kuwa shi ne mahaifin Eber.
19 Aka haifa wa Eber ʼyaʼya maza biyu.
Aka kira ɗaya Feleg domin a lokacinsa ne aka raba duniya; sunan ɗanʼuwansa kuwa shi ne Yoktan.
20 Yoktan shi ne mahaifin

---

* **1:4** Seftuwajin; Ibraniyanci ba su da ʼYaʼyan Nuhu maza. † **1:5** ʼYaʼya suna iya nufin zuriya Ko kuwa magāda ko alʼummai; haka ma a ayoyi 6-10, 17 da 20. ‡ **1:6** Yawancin rubuce-rubucen hannu na Ibraniyanci da na Bulget (dubi kuma Seftuwajin da Far 10.3); yawancin rubuce-rubucen hannu na Ibraniyanci suna da Difat § **1:8** Wato, Masar; haka ma a aya ta 11. * **1:10** Mahaifi na iya nufin kaka ko wanda ya riga Ko kuwa wanda yake tushe; haka ma a ayoyi 11, 13, 18 da 20.

Almodad, Shelef, Hazarmawet, Yera 21 Hadoram, Uzal, Dikla, 22 Ebal, Abimayel,
Sheba, 23 Ofir, Hawila da Yobab. Dukan waɗannan ʼyaʼyan Yoktan maza ne.

### *Zuriyar Shem*
### *(Farawa 11.10-26)*

24 Shem, Arfakshad,† Shela,
25 Eber, Feleg, Reyu
26 Serug, Nahor, Tera
27 da Abram (wato, Ibrahim).

### *Iyalin Ibrahim*
### *(Farawa 25.1-4,12-16)*

28 ʼYaʼyan Ibrahim maza su ne, Ishaku da Ishmayel.

### *Zuriyar Hagar*

29 Waɗannan su ne zuriyarsu.
Nebayiwot ɗan farin Ishmayel, Kedar, Adbeyel, Mibsam, 30 Mishma, Duma, Massa,
Hadad, Tema 31 Yetur, Nafish da Kedema.
Waɗannan su ne ʼyaʼyan Ishmayel maza.

### *Zuriyar Ketura*

32 ʼYaʼyan Ketura maza, ƙwarƙwarar Ibrahim su ne,
Zimran, Yokshan, Medan, Midiyan, Ishbak da Shuwa.
ʼYaʼyan Yokshan maza su ne,
Sheba da Dedan.
33 ʼYaʼyan Midiyan maza su ne,
Efa, Efer, Hanok, Abida da Eldaʼa.
Dukan waɗannan su ne zuriyar Ketura.

### *Zuriyar Saratu*

34 Ibrahim shi ne mahaifin Ishaku.
ʼYaʼyan Ishaku maza su ne,
Isuwa da Israʼila.

### *ʼYaʼyan Isuwa maza*
### *(Farawa 36.1-14)*

35 ʼYaʼyan Isuwa maza, su ne,
Elifaz, Reyuwel, Yewush, Yalam da Kora
36 ʼYaʼyan Elifaz maza su ne,
Teman, Omar, Zefi, Gatam, Kenaz,
da Timna wanda aka haifa wa Amalek.‡
37 ʼYaʼyan maza Reyuwel su ne,
Nahat, Zera, Shamma da Mizza.

### *Mutanen Seyir a Edom*
### *(Farawa 36.20-43)*

38 ʼYaʼyan Seyir maza su ne,
Lotan, Shobal, Zibeyon, Ana, Dishon, Ezer da Dishan.
39 ʼYaʼyan Lotan maza su ne,
Hori da Homam. Timna ita ce ʼyarʼuwar Lotan.
40 ʼYaʼyan Shobal maza su ne,
Alwan, Manahat, Ebal, Shefo da Onam.

---

† **1:24** Da Ibraniyanci; waɗansu rubuce-rubucen hannu na Seftuwajin suna da Arfakshad, Kainan (dubi kuma sharhi a Far 11.10). ‡ **1:36** Waɗansu rubuce-rubucen hannun Seftuwajin (dubi Far 36.12); Ibraniyanci yana da Gatam, Kenaz, Timna da Amalek

ʼYaʼyan Zibeyon maza su ne,
Aiya da Ana.
41 Ɗan Ana shi ne,
Dishon.
ʼYaʼyan Dishon maza su ne,
Hemdan, Eshban, Itran da Keran.
42 ʼYaʼyan Ezer maza su ne,
Bilhan, Zaʼaban da Yaʼakan.
ʼYaʼyan Dishan maza su ne,
Uz da Aran.

*Masu mulkin Edom*

43 Waɗannan su ne sarakunan da suka yi sarauta a Edom kafin wani sarkin
mutumin Israʼila yă yi sarauta.
Bela ɗan Beyor, wanda aka kira birninsa Dinhaba.
44 Saʼad da Bela ya mutu sai Yobab ɗan Zera daga Bozra ya gāje shi a matsayin
sarki.
45 Da Yobab ya mutu, Husham daga ƙasar Temaniyawa ya gāje shi a matsayin sarki.
46 Saʼad da Husham ya mutu, Hadad ɗan Bedad, wanda ya ci Midiyan da yaƙi a
cikin ƙasar Mowab, ya gāje shi a matsayin sarki. Aka kira birninsa Awit.
47 Da Hadad ya mutu, Samla daga Masreka ya gāje shi a matsayin sarki.
48 Saʼad da Samla ya mutu, Shaʼul daga Rehobot na kogi ya gāje shi a matsayin
sarki.
49 Saʼad da Shaʼul ya mutu, Baʼal-Hanan ɗan Akbor ya gāje shi a matsayin sarki.
50 Saʼad da Baʼal-Hanan ya mutu, Hadad ya gāje shi a matsayin sarki. Aka kira
birninsa Fau, sunan matarsa kuwa Mehetabel ʼyar Matired, ʼyar Me-Zahab.
51 Hadad shi ma ya mutu.

Manyan Edom su ne,
Timna, Alwa, Yetet 52 Oholibama, Ela, Finon 53 Kenaz, Teman, Mibzar, 54 Magdiyel
da Iram.
Waɗannan su ne manyan Edom.

# 2

*ʼYaʼyan Israʼila maza*

1 Waɗannan su ne ʼyaʼyan Israʼila maza. Ruben, Simeyon, Lawi, Yahuda,
Issakar, Zebulun, 2 Dan, Yusuf, Benyamin, Naftali, Gad da Asher.

*Zuriyar Yahuda*

*ʼYaʼyan Hezron maza*

3 ʼYaʼyan Yahuda maza su ne,
Er, Onan da Shela. Waɗannan mutum uku Bat-shuwa mutuniyar Kanʼana ce ta haifa masa.
Er, ɗan farin Yahuda mugu ne a gaban Ubangiji, saboda haka Ubangiji ya kashe shi.
4 Tamar, surukar Yahuda, ta haifa masa Ferez da Zera.
Yahuda ya haifi ʼyaʼya maza biyar ne.

5 ʼYaʼyan Ferez maza su ne,
Hezron da Hamul.
6 ʼYaʼyan Zera maza su ne,
Zimri, Etan, Heman, Kalkol da Darda, su biyar ne.

7 ʼYaʼyan Karmi maza su ne,
Akar* wanda ya kawo masifa wa Isra'ila ta wurin yin abin da aka haramta.
8 Ɗan Etan shi ne,
Azariya.
9 ʼYaʼya maza da aka haifa wa Hezron su ne,
Yerameyel, Ram da Kaleb.

*Daga Ram ɗan Hezron*

10 Ram shi ne mahaifin Amminadab,
Amminadab kuwa shi ne mahaifin Nashon, shugaban mutanen Yahuda.
11 Nashon shi ne mahaifin Salma,
Salma shi ne mahaifin Bowaz,
12 Bowaz shi ne mahaifin Obed
kuma Obed shi ne mahaifin Yesse.

13 Yesse shi ne mahaifin.
Eliyab ɗan farinsa, ɗansa na biyu shi ne Abinadab,
na ukun Shimeya, 14 na huɗun Netanel,
na biyar Raddai, 15 na shidan Ozem
na bakwai kuma Dawuda.
16 ʼYanʼuwansu mata su ne Zeruhiya da Abigiyel.
ʼYaʼyan Zeruhiya maza guda uku su ne Abishai, Yowab da Asahel.
17 Abigiyel ita ce mahaifiyar Amasa, wanda mahaifinsa shi ne Yeter mutumin Ishmayel.

*Zuriyar Kaleb ɗan Hezron*

18 Kaleb ɗan Hezron ya haifi yara ta wurin matarsa Azuba (da kuma ta wurin Yeriyot). Waɗannan su ne ʼyaʼyan Azuba maza.
Yesher, Shobab da Ardon.
19 Da Azuba ta mutu, Kaleb ya auri Efrat, wadda ta haifa masa Hur.
20 Hur shi ne mahaifin Uri, Uri kuma shi ne mahaifin Bezalel.

21 Daga baya, Hezron ya kwana da ʼyar Makir mahaifin Gileyad (ya aure ta saʼad da take da shekara sittin), ta haifa masa Segub.
22 Segub shi ne mahaifin Yayir, wanda ya yi mulkin garuruwa uku a Gileyad.
23 (Amma Geshur da Aram suka ƙwace Hawwot Yayir da kuma Kenat tare da ƙauyukan kewayenta, garuruwa sittin.)
Dukan waɗannan su ne zuriyar Makir mahaifin Gileyad.
24 Bayan Hezron ya mutu a Kaleb Efrata, sai Abiya matar Hezron ta haifa masa Asshur mahaifin Tekowa.

*Zuriyar Yerameyel ɗan Hezron*

25 ʼYaʼyan Yerameyel maza, ɗan farin Hezron su ne,
Ram shi ne ɗan fari, sai Buna, Oren, Ozem da Ahiya. 26 Yerameyel yana da wata mata, wadda sunanta Atara; ita ce mahaifiyar Onam.
27 ʼYaʼyan Ram maza ɗan farin Yerameyel su ne,
Maʼaz, Yamin da Eker.
28 ʼYaʼyan Onam maza su ne,
Shammai da Yada.
ʼYaʼyan Shammai maza su ne,

* **2:7** Akar yana nufin masifa; Akar an kira shi Akan a cikin Yoshuwa.

Nadab da Abishur. 29 Sunan matar Abishur ita ce Abihayil, wadda ta haifa masa
Aban da Molid.
30 ʼYaʼyan Nadab maza su ne,
Seled da Affayim. Seled ya mutu babu yara.
31 Ɗan Affayim shi ne,
Ishi, wanda shi ne mahaifin Sheshan. Sheshan shi ne mahaifin Alai.
32 ʼYaʼyan Yada maza, ɗanʼuwan Shammai su ne,
Yeter da Yonatan. Yeter ya mutu babu yara.
33 ʼYaʼyan Yonatan maza su ne,
Felet da Zaza.
Waɗannan su ne zuriyar Yerameyel.

34 Sheshan ba shi da ʼyaʼya maza, sai ʼyaʼya mata kawai.
Yana da bawa mutumin Masar mai suna Yarha. 35 Sheshan ya ba da ʼyarsa aure
ga bawansa Yarha, ta kuwa haifa masa Attai.
36 Attai shi ne mahaifin Natan,
Natan shi ne mahaifin Zabad,
37 Zabad shi ne mahaifin Eflal,
Eflal shi ne mahaifin Obed,
38 Obed shi ne mahaifin Yehu,
Yehu shi ne mahaifin Azariya,
39 Azariya shi ne mahaifin Helez,
Helez shi ne mahaifin Eleyasa,
40 Eleyasa shi ne mahaifin Sismai,
Sismai shi ne mahaifin Shallum
41 Shallum shi ne mahaifin Yekamiya,
Yekamiya kuma shi ne mahaifin Elishama.

### *Gidan Kaleb*

42 ʼYaʼyan Kaleb maza, ɗanʼuwan Yerameyel su ne,
Mesha ɗan farinsa, wanda shi ne mahaifin Zif,
da ɗansa Maresha, wanda shi ne mahaifin Hebron.
43 ʼYaʼyan Hebron maza su ne,
Kora, Taffuwa, Rekem da Shema.
44 Shema shi ne mahaifin Raham,
Raham kuma shi ne mahaifin Yorkeyam.
Rekem shi ne mahaifin Shammai.
45 Ɗan Shammai shi ne Mawon,
Mawon kuma shi ne mahaifin Bet-Zur.
46 Efa ƙwarƙwarar Kaleb ita ce mahaifiyar
Haran, Moza da Gazez.
Haran shi ne mahaifin Gazez.
47 ʼYaʼyan Yadai maza su ne,
Regem, Yotam, Geshan, Felet, Efa da Shaʼaf.
48 Maʼaka ƙwarƙwarar Kaleb ita ce mahaifiyar
Sheber da Tirhana.
49 Ta kuma haifi Shaʼaf mahaifin Madmanna
da kuma Shewa, mahaifin Makbena da Gibeya.
ʼYar Kaleb ita ce Aksa.
50 Waɗannan su ne zuriyar Kaleb.

ʼYaʼyan Hur maza, ɗan farin Efrata su ne,

Shobal mahaifin Kiriyat Yeyarim, 51 Salma mahaifin Betlehem, da kuma Haref mahaifin Bet-Gader.
52 Zuriyar Shobal mahaifin Kiriyat Yeyarim su ne,
Harowe, rabin Manahatiyawa, 53 kuma gidan Kiriyat Yeyarim su ne, Itrayawa, Futiyawa, Shumatiyawa da Mishratiyawa. Daga waɗannan ne Zoratiyawa da Eshtawoliyawa suka fito.
54 Zuriyar Salma su ne,
Betlehem, Netofawa, Atrot Bet Yowab, rabin Manahatiyawa, Zoriyawa, 55 kuma gidan marubuta waɗanda suke zama a Yabez su ne, Tiratiyawa, Shimeyatiyawa da Sukatiyawa. Waɗannan su ne Keniyawa waɗanda suka zo daga Hammat, mahaifin gidan Rekab.

# 3

*ʼYaʼyan Dawuda maza*

1 Waɗannan su ne ʼyaʼyan Dawuda maza da aka haifa masa a Hebron.

Ɗan farinsa shi ne Amnon ɗan Ahinowam mutuniyar Yezireyel;
na biyun, Daniyel ɗan Abigiyel mutuniyar Karmel;
2 na ukun, Absalom ɗan Maʼaka ʼyar Talmai sarkin Geshur;
na huɗun, Adoniya ɗan Haggit;
3 na biyar, Shefatiya ɗan Abital;
da kuma na shida, Itireyam ta wurin matarsa Egla.

4 Waɗannan su ne aka haifa wa Dawuda a Hebron, inda ya yi mulki shekaru bakwai da wata shida.

Dawuda ya yi mulki a Urushalima shekaru talatin da uku, 5 kuma waɗannan su ne yaran da aka haifa masa a can.

Shimeya,* Shobab, Natan da Solomon. Waɗannan huɗu ne Bat-shuwa† ʼyar Ammiyel ta haifa.
6 Akwai kuma Ibhar, Elishama, Elifelet, 7 Noga, Nefeg, Yafiya, 8 Elishama, Eliyada da Elifelet, su tara ne duka.

9 Dukan waɗannan ʼyaʼyan Dawuda ne maza, ban da ʼyaʼyansa maza ta wurin ƙwarƙwaransa. Tamar ita ce ʼyarʼuwarsu.

*Sarakuna Yahuda*

10 Zuriyar Solomon su ne Rehobowam,
da Abiya,
da Asa,
da Yehoshafat,
11 da Yoram‡,
da Ahaziya,
da Yowash,
12 da Amaziya,
da Azariya,
da Yotam,

* **3:5** Da Ibraniyanci Shimeya, wani suna na Shammuwa † **3:5** Bat-shuwa. Waɗansu tsofaffin fassarori biyu (duba kuma 2Sam 11); Ibraniyanci yana da “Batsheba” ne a nan. ‡ **3:11** Da Ibraniyanci Yoram, wani suna na Yehoram

13 da Ahaz,
da Hezekiya
da Manasse,
14 da Amon,
da Yosiya.
15 'Ya'yan Yosiya maza su ne,
Yohanan ɗan fari,
Yehohiyakim ɗa na biyu,
Zedekiya ɗa na uku
Shallum ɗa na huɗu.
16 Magādan Yehohiyakim§ su ne,
Yekoniya ɗansa,
da Zedekiya.

*Zuriyar sarauta bayan zaman bauta*

17 Zuriyar Yekoniya kamamme su ne,
Sheyaltiyel, 18 Malkiram, Fedahiya, Shenazzar, Yekamiya, Hoshama da Nedabiya.
19 'Ya'yan Fedahiya su ne,
Zerubbabel da Shimeyi.
'Ya'yan Zerubbabel maza su ne,
Meshullam da Hananiya. Shelomit ce 'yar'uwarsu. 20 Akwai kuma waɗansu biyar,
Hashuba, Ohel, Berekiya, Hasadiya da Yushab-Hesed.
21 Zuriyar Hananiya su ne,
Felatiya da Yeshahiya, Refahiya, Arnan, Obadiya da Shekaniya.
22 Zuriyar Shekaniya su ne,
Shemahiya da 'ya'yansa maza. Hattush, Igal, Bariya, Neyariya da Shafat, su shida ne duka.
23 'Ya'yan Neyariya maza su ne,
Eliyohenai, Hezekiya da Azrikam, su uku ne duka.
24 'Ya'yan Eliyohenai su ne,
Hodawiya, Eliyashib, Felahiya, Akkub, Yohanan, Delahiya da Anani, su bakwai ne duka.

# 4

*Sauran gidajen Yahuda*

1 Zuriyoyin Yahuda su ne,
Ferez, Hezron, Karmi, Hur da Shobal.
2 Reyahiya ɗan Shobal shi ne mahaifin Yahat, Yahat shi ne mahaifin Ahumai da Lahad. Waɗannan su ne gidajen Zoratiyawa.
3 Waɗannan su ne 'ya'yan Etam.
Yezireyel, Ishma da Idbash. 'Yar'uwarsu ita ce Hazzelelfoni. 4 Fenuwel shi ne mahaifin Gedor, kuma Ezer shi ne mahaifin Husha.
Waɗannan su ne zuriyar Hur, ɗan farin Efrata da mahaifin Betlehem.
5 Asshur mahaifin Tekowa yana da mata biyu, Hela da Na'ara.
6 Na'ara ta haifi Ahuzzam, Hefer, Temeni da Hawahashtari. Waɗannan su ne zuriyar Na'ara.
7 'Ya'yan Hela maza su ne,
Zeret, Zohar, Etnan, 8 da Koz. Koz ne mahaifin Anub da Hazzobeba, shi ne kuma kakan iyalin da suka fito daga zuriyar Aharhel ɗan Harum.

§ **3:16** Da Ibraniyanci Yekoniya, wani suna na Yekoniya; haka kuma a aya 17.

[9] Yabez ya fi ʼyanʼuwansa martaba. Mahaifiyarsa ta sa masa suna Yabez, tana cewa,
"Na haife shi da azaba." [10] Yabez ya yi kuka ga Allah na Israʼila ya ce, "Ka yi mini
albarka ka fadada yankina! Bari hannunka yă kasance tare da ni, yă kuma kiyaye ni
daga abin da zai cuce ni, don kada in shiga wahala." Sai Allah ya ji roƙonsa.

[11] Kelub, ɗanʼuwan Shuha, shi ne mahaifin Mehir, wanda shi ne mahaifin Eshton.
[12] Eshton shi ne mahaifin Bet-Rafa, Faseya da Tehinna wanda ya haifi Ir Nahash.
Waɗannan su ne mutanen Reka.

[13] ʼYaʼyan Kenaz maza su ne,
Otniyel da Serahiya.
ʼYaʼyan Otniyel maza su ne,
Hatat da Meyonotai. [14] Meyonotai shi ne mahaifin Ofra.
Serahiya shi ne mahaifin Yowab,
mahaifin Ge-Harashim. An kira shi haka domin mutanensa masu sanaʼar hannu ne.
[15] ʼYaʼyan Kaleb ɗan Yefunne maza su ne,
Iru, Ela da Naʼam.
Ɗan Ela shi ne,
Kenaz.
[16] ʼYaʼyan Yahallelel su ne,
Zif, Zifa, Tiriya da Asarel.
[17] ʼYaʼyan Ezra maza su ne,
Yeter, Mered, Efer da Yalon.
Ɗaya daga cikin matan Mered ta haifi Miriyam, Shammai da Ishba wanda ya haifi Eshtemowa.
[18] (Matarsa mutuniyar Yahuda kuwa ta haifi Yared mahaifin Gedor, Heber mahaifin Soko, da kuma Yekutiyel mahaifin Zanowa.) Waɗannan su ne ʼyaʼyan Bitiya ʼyar Firʼauna, wadda Mered ya aura.
[19] ʼYaʼyan matar Hodiya, ʼyarʼuwar Naham su ne,
suka haifi Keyila Bagarme, da Eshtemowa mutumin Maʼaka.
[20] ʼYaʼyan Shimon maza su ne,
Amnon, Rinna, Ben-Hanan da Tilon.
Zuriyar Ishi su ne,
Zohet da Ben-Zohet.
[21] ʼYaʼyan Shela ɗan Yahuda maza su ne,
Er mahaifin Leka, Laʼada mahaifin Maresha da kuma gidajen masu aikin lilin a Bet-Ashbeya,
[22] da Yokim, mutanen Kozeba, da Yowash da Saraf wanda ya yi mulkin Mowab
da kuma Yashubi Lehem (Waɗannan rubutattun tarihi ne na tun dā.) [23] Su ne
maginan tukwane waɗanda suka zauna a Netayim da Gedera; sun zauna a can suka kuma yi wa sarki aiki.

### *Zuriyar Simeyon*

[24] Zuriyar Simeyon su ne,
Nemuwel, Yamin, Yarib, Zera da Shawulu;
[25] Shawulu ya haifi Shallum, Shallum ya haifi Mibsam. Mibsam ya haifi Mishma.
[26] Zuriyar Mishma su ne,
Hammuwel ɗansa, wanda ya haifi Zakkur, shi Zakkur kuma ya haifi Shimeyi.

[27] Shimeyi yana da ʼyaʼya maza goma sha shida da ʼyaʼya mata shida, amma
ʼyanʼuwansa ba su da ʼyaʼya da yawa; saboda haka gidansu gaba ɗaya ba tă zama

mai mutane da yawa kamar mutanen Yahuda ba. 28 Sun zauna a Beyersheba, Molada,
Hazar Shuwal, 29 Bilha, Ezem, Tolad 30 Betuwel, Horma, Ziklag, 31 Bet-Markabot,
Hazar-Susim, Bet-Biri da Sha'arayim. Waɗannan su ne garuruwansu har lokacin
mulkin Dawuda. 32 Kauyukan da suke kewayensu su ne Etam, Ayin, Rimmon,
Token da Ashan, garuruwa biyar; 33 da kuma dukan ƙauyuka kewaye da waɗannan
garuruwa har zuwa Ba'al. Waɗannan ne wuraren zamansu.

Suka kuma ajiye tarihin zuriya.

34 Zuriyar Simeyon ta ƙunshi Meshobab, da Yamlek,
da Yosha ɗan Amaziya. 35 Akwai Yowel,
da Yehu ɗan Yoshibiya. Yoshibiya ɗan Seraya ne. Serahiya kuma ɗan Asiyel ne.
36 Akwai Eliyohenai da Ya'akoba, da Yeshohahiya,
da Asahiya, da Adiyel, da Yesimiyel, da Benahiya.
37 Akwai Ziza ɗan Shifi. Shifi ɗan Allon ne. Allon ɗan Yedahiya ne. Yedahiya ɗan Shimri ne. Shimri kuma ɗan Shemahiya ne.

38 Mutanen da aka jera sunayensu a bisa, shugabannin gidajensu ne.

Iyalansu sun ƙaru sosai, 39 suka tafi bayan garin Gedor wajajen gabashin kwari
suna neman makiyaya domin garkunansu. 40 Suka sami makiyaya mai ciyawa mai
kyau, ƙasar kuma tana da fāɗi, da salama, kuma zaman lafiya. A dā waɗansu
mutanen Ham sun zauna a can.
41 Mutanen da aka jera sunayensu sun zo ne a zamanin Hezekiya sarkin Yahuda.
Suka yaƙi mutanen Ham a wuraren zamansu, haka kuma suka yi da Meyunawa
da suke can, suka hallaka su ƙaƙaf, yadda yake har yă zuwa yau. Sa'an nan suka
zauna a wurin, gama akwai makiyaya domin garkunansu. 42 Mutum ɗari biyar
na waɗannan mutane Simeyon, waɗanda Felatiya, Neyariya, Refahiya da Uzziyel,
'ya'yan Ishi maza suka jagorance, sun mamaye ƙasar tudu ta Seyir. 43 Suka karkashe
raguwar Amalekawan da suka tsere, suka kuma zauna a can har yă zuwa yau.

# 5

*Zuriyar Ruben*

1 'Ya'yan Ruben maza ɗan farin Isra'ila (shi ne ɗan fari, amma sa'ad da ya ƙazantar da gadon auren mahaifinsa, sai aka ba wa 'yancin ɗan farinsa wa 'ya'yan Yusuf maza ɗan Isra'ila; don kada a lissafta shi a tarihin zuriya bisa ga matsayin haihuwarsa, 2 ko da yake Yahuda shi ne mafi ƙarfi cikin 'yan'uwansa kuma mai mulki ya fito daga gare shi, 'yancin zaman ɗan fari na Yusuf ne), 3 'ya'yan Ruben ɗan farin Isra'ila maza su ne,

Hanok, Fallu, Hezron da Karmi.
4 Zuriyar Yowel su ne,
Shemahiya, Gog,
Shimeyi, 5 Mika,
Reyahiya, Ba'al,
6 da Beyera, wanda Tiglat-Fileser sarkin Assuriya ya ɗauka zuwa zaman bauta. Beyera shi ne shugaban mutanen Ruben.
7 Danginsu bisa ga iyalansu da aka jera bisa ga tarihin zuriyarsu su ne,
Yehiyel shi ne sarki, akwai Zakariya, 8 da Bela ɗan Azaz. Azaz ɗan Shema daga dangin Yowel.

Yowel ya yi zama a yankin Arower har zuwa Nebo da Ba'al-Meyon. 9 Ta waje gabas
sun zauna a ƙasar har zuwa bakin hamadan da ya nausa zuwa Kogin Yuferites, domin
dabbobinsu sun ƙaru a Gileyad.
10 A zamanin Shawulu zuriyar Ruben sun yi yaƙi da Hagirawa, suka ci su da yaƙi,
suka zauna a wuraren zaman Hagirawan ko'ina a dukan yankin gabashin Gileyad.

### *Zuriyar Gad*

11 Mutanen Gad sun zauna kusa da mutanen Ruben a Bashan, har zuwa Saleka.

12 Yowel shi ne babba, sai Shafan na biyu, sa'an nan Yanai da Shafat, su ne tushen Bashan.
13 Danginsu, bisa ga iyalai su ne,
Mika'ilu, Meshullam, Sheba, Yorai, Yakan, Ziya da Eber, su bakwai ne duka.
14 Waɗannan su ne 'ya'yan Abihayil ɗan Huri, ɗan Yarowa, ɗan Gileyad, ɗan Mika'ilu, ɗan Yeshishai, ɗan Yado, ɗan Buz.
15 Ahi ɗan Abiyel, ɗan Guni, shi ne kan iyalinsu.

16 Mutanen Gad sun zauna a Bashan da ƙauyukan da suke kurkusa da shi, da kuma
a dukan makiyayan Sharon har zuwa iyaka inda suka kai.
17 Dukan waɗannan sun shiga tarihin zuriya a lokacin mulkin Yotam sarkin Yahuda
da Yerobowam sarkin Isra'ila.

18 Mutanen Ruben, mutanen Gad da rabin kabilar Manasse sun kasance da mutane
44,760 shiryayyu don aikin soja, jarumawan da za su iya riƙe garkuwa da takobi,
waɗanda suke iya yin amfani da baka, waɗanda kuma aka horar don yaƙi. 19 Suka
yi yaƙi da Hagirawa, Yetur, Nafish da Nodab. 20 Aka taimake su a yaƙin, Allah kuma
ya ba da Hagirawa da dukan abokansu gare su, domin sun yi kuka gare shi a lokacin
yaƙin. Ya amsa addu'o'insu, domin sun dogara gare shi. 21 Suka ƙwace dabbobin
Hagirawa, raƙuma dubu hamsin, tumaki dubu ɗari biyu da hamsin da kuma jakuna
dubu biyu. Suka kuma kame mutane dubu ɗari ɗaya, 22 waɗansu suka mutu, domin
yaƙin na Allah ne. Suka zauna a ƙasar har lokacin da aka kai su zaman bauta.

### *Rabin kabilar Manasse*

23 Mutanen rabin kabilar Manasse sun yi yawa; suka zauna a ƙasar daga Bashan
har zuwa Ba'al-Hermon, wato, zuwa Senir (Dutsen Hermon).
24 Waɗannan su ne kawunan iyalansu. Efer, Ishi, Eliyel, Azriyel, Irmiya, Hodawiya
da Yadiyel. Su jarumawa ne, sanannu, su ne kuma kawunan iyalansu. 25 Amma ba
su yi aminci da Allahn kakanninsu ba, suka kuma yi karuwanci ga waɗansu allolin
mutanen ƙasar, waɗanda Allah ya hallaka a gabansu. 26 Saboda haka Allah na Isra'ila
ya zuga ruhun Ful sarkin Assuriya (wato, Tiglat-Fileser sarkin Assuriya), wanda ya
kwashe mutanen Ruben, mutanen Gad da rabin kabilar Manasse zuwa zaman bauta.
Ya kwashe su zuwa Hala, Habor, Hara da kuma kogin Gozan, inda suke har wa yau.

## 6

### *Zuriyar Lawi*

1 'Ya'yan Lawi maza su ne,
Gershon, Kohat da Merari.
2 'Ya'yan Kohat maza su ne,
Amram, Izhar, Hebron da Uzziyel.
3 Yaran Amram su ne,
Haruna, Musa da Miriyam.

ʼYaʼyan Haruna maza su ne,
Nadab, Abihu, Eleyazar da Itamar.
4 Eleyazar shi ne mahaifin Finehas,
Finehas mahaifin Abishuwa,
5 Abishuwa mahaifin Bukki,
Bukki mahaifin Uzzi,
6 Uzzi mahaifin Zerahiya,
Zerahiya mahaifin Merahiyot,
7 Merahiyot mahaifin Amariya,
Amariya mahaifin Ahitub,
8 Ahitub mahaifin Zadok,
Zadok mahaifin Ahimawaz,
9 Ahimawaz mahaifin Azariya,
Azariya mahaifin Yohanan,
10 Yohanan mahaifin Azariya (shi ne ya yi hidima a matsayin firist a haikalin da Solomon ya gina a Urushalima),
11 Azariya mahaifin Amariya,
Amariya mahaifin Ahitub,
12 Ahitub mahaifin Zadok,
Zadok mahaifin Shallum,
13 Shallum mahaifin Hilkiya,
Hilkiya mahaifin Azariya,
14 Azariya mahaifin Serahiya,
Serahiya kuwa mahaifin Yehozadak.
15 Yehozadak ne aka ɗauka saʼad da UBANGIJI ya tura Yahuda da Urushalima zuwa zaman bauta ta hannun Nebukadnezzar.

16 ʼYaʼyan Lawi maza su ne,
Gershom, Kohat da Merari.
17 Waɗannan su ne sunayen ʼyaʼyan Gershom.
Libni da Shimeyi.
18 ʼYaʼyan Kohat maza su ne,
Amram, Izhar, Hebron da Uzziyel.
19 ʼYaʼyan Merari maza su ne,
Mali da Mushi.

Waɗannan suke gidajen Lawiyawan da aka jera bisa ga kakanninsu.
20 Na Gershom su ne,
Libni, Yahat,
Zimma, 21 Yowa,
Iddo, Zera
da Yeyaterai.
22 Zuriyar Kohat su ne,
Amminadab, Kora,
Assir, 23 Elkana,
Ebiyasaf, Assir,
24 Tahat, Uriyel,
Uzziya da Shawulu.
25 Zuriyar Elkana su ne,
Amasai, Ahimot,
26 Elkana, Zofai,

Nahat, 27 Eliyab
Yeroham, Elkana
da Sama'ila.
28 'Ya'yan Sama'ila maza su ne,
Yowel ɗan fari
da Abiya ɗa na biyu.
29 Zuriyar Merari su ne,
Mali, Libni,
Shimeyi, Uzza,
30 Shimeya, Haggiya
da Asahiya.

*Mawaƙan haikali*

31 Waɗannan su ne mutanen da Dawuda ya sa su lura da waƙa a cikin gidan
UBANGIJI bayan da aka kawo akwatin alkawari yă huta a can. 32 Suka yi hidima
da waƙa a gaban tabanakul, Tentin Sujada, sai da Solomon ya gina haikalin UBANGIJI
a Urushalima. Suka yi ayyukansu bisa ga ƙa'idodin da aka shimfiɗa musu.

33 Ga mutanen da suka yi hidimar, tare da 'ya'yansu maza.

Daga mutanen Kohat akwai,
Heman, mawaƙi
ɗan Yowel, ɗan Sama'ila,
34 ɗan Elkana, ɗan Yeroham,
ɗan Eliyel, ɗan Towa,
35 ɗan Zuf, ɗan Elkana,
ɗan Mahat, ɗan Amasai,
36 ɗan Elkana, ɗan Yowel,
ɗan Azariya, ɗan Zefaniya
37 ɗan Tahat, ɗan Assir,
ɗan Ebiyasaf, ɗan Kora,
38 ɗan Izhar, ɗan Kohat,
ɗan Lawi, ɗan Isra'ila;
39 da kuma Asaf 'yan'uwan Heman, waɗanda suka yi hidima a hannun damansa.
Asaf ɗan Berekiya, ɗan Shimeya,
40 ɗan Mika'ilu, ɗan Ba'asehiya,
ɗan Malkiya, 41 ɗan Etni,
ɗan Zera, ɗan Adahiya
42 ɗan Etan, ɗan Zimma,
ɗan Shimeyi, 43 ɗan Yahat,
ɗan Gershom, ɗan Lawi;
44 da kuma daga 'yan'uwansu, mutanen Merari, a hannun hagunsa.
Etan ɗan Kishi, ɗan Abdi,
ɗan Malluk, 45 ɗan Hashabiya,
ɗan Amaziya, ɗan Hilkiya,
46 ɗan Amzi, ɗan Bani,
ɗan Shemer, 47 ɗan Mali,
ɗan Mushi, ɗan Merari,
ɗan Lawi.

48 Aka ba 'yan'uwansu Lawiyawa dukan sauran ayyukan tabanakul, gidan Allah.
49 Amma Haruna da zuriyarsa su ne waɗanda suke miƙa hadayu a kan bagaden
hadaya ta ƙonawa da kuma a kan bagaden turare haɗe da dukan abin da ake yi a

Wuri Mafi Tsarki, suna yin kafara domin Isra'ila, bisa ga dukan abin da Musa bawan Allah ya umarta.

50 Waɗannan su ne zuriyar Haruna,
Eleyazar, Finehas,
Abishuwa, 51 Bukki,
Uzzi, Zerahiya,
52 Merahiyot, Amariya,
Ahitub, 53 Zadok
da Ahimawaz.

*(Yoshuwa 21.1-42)*

54 Waɗannan su ne wuraren zamansu da aka ba su rabo su zama yankunansu (aka ba wa zuriyar Haruna waɗanda suke daga gidan Kohat, domin rabo na fari nasu ne):
55 Aka ba su Hebron a Yahuda tare da wuraren kiwon da suke kewayenta. 56 Amma
filaye da ƙauyukan da suke kewayen birnin aka ba wa Kaleb ɗan Yefunne.
57 Saboda haka aka ba wa zuriyar Haruna Hebron (birnin mafaka), da Libna,
Yattir Eshtemowa, 58 Hilen, Debir, 59 Ashan, Yutta da Bet-Shemesh, tare da
wuraren kiwonsu.
60 Daga kabilar Benyamin kuma aka ba su Gibeyon, Geba, Alemet da Anatot, tare da wuraren kiwonsu.

Waɗannan garuruwa waɗanda aka raba a tsakanin mutanen gidan Kohat, goma sha uku ne duka.

61 Aka ba sauran zuriyar Kohat rabon garuruwa goma daga gidajen rabin kabilar Manasse.
62 Aka ba zuriyar Gershom, gida-gida, rabon garuruwa goma sha uku daga kabilan Issakar, Asher da Naftali, da kuma daga sashen rabi kabilar Manasse da yake a Bashan.
63 Aka ba zuriyar Merari, gida-gida, rabon garuruwa goma sha biyu daga kabilan Ruben, Gad da Zebulun.

64 Saboda haka Isra'ilawa suka ba Lawiyawa waɗannan garuruwa da wuraren kiwonsu.

65 Daga kabilan Yahuda, Simeyon da Benyamin suka ba su rabon sunayen garuruwan da aka ambata.

66 Aka ba wa waɗansu na mutanen gidan Kohat yankin garuruwansu daga kabilar Efraim.
67 A ƙasar tudun Efraim aka ba su Shekem (birnin mafaka), da Gezer, 68 Yokmeyam,
Bet-Horon, 69 Aiyalon da Gat-Rimmon, tare da wuraren kiwonsu.
70 Daga rabin kabilar Manasse kuwa, Isra'ilawa suka ba da Aner da Bileyam, tare da wuraren kiwonsu, ga sauran gidajen mutanen Kohat.

71 Mutanen Gershom suka sami waɗannan.

Daga gidan rabin kabilar Manasse, sun sami Golan a Bashan da kuma Ashtarot, tare da wuraren kiwonsu;
72 daga kabilar Issakar suka sami Kedesh, Daberat, 73 Ramot da Anem, tare da
wuraren kiwonsu;
74 daga kabilar Asher suka sami Mashal, Abdon, 75 Hukok da Rehob, tare da wuraren
kiwonsu;

76 daga kabilar Naftali kuwa suka sami Kedesh a Galili, Hammon da Kiriyatayim, tare da wuraren kiwonsu.

77 Mutanen Merari (sauran Lawiyawan) suka sami waɗannan.
Daga kabilar Zebulun suka sami Yokneyam, Karta, Rimmon da Tabor, tare da wuraren kiwonsu;
78 daga kabilar Ruben a hayin Urdun a gabashi Yeriko suka sami Bezer a hamada,
Yahza, 79 Kedemot da Mefa'at, tare da wuraren kiwonsu;
80 daga kabilar Gad kuwa suka sami Ramot a Gileyad, Mahanayim, 81 Heshbon da
Yazer, tare da wuraren kiwonsu.

# 7

*Zuriyar Issakar*

1 'Ya'yan Issakar maza su ne,
Tola, Fuwa, Yashub da Shimron, su huɗu ne duka.
2 'Ya'yan Tola maza su ne,
Uzzi, Refahiya, Yeriyel, Ibsam da Sama'ila, su ne kuma kawunan iyalansu. A zamanin mulkin Dawuda, an rubuta zuriyar Tola a matsayin mayaƙa a cikin tarihinsu, sun kai 22,600.
3 Ɗan Uzzi shi ne,
Izrahiya.
'Ya'yan Izrahiya maza su ne,
Mika'ilu, Obadiya, Yowel da Isshiya. Dukansu biyar manya ne. 4 Bisa ga tarihin
iyalinsu, sun kai mutane 36,000 shiryayyu don yaƙi, gama suna da mata da 'ya'ya da yawa.
5 Dangin da suke maza masu yaƙi sun kasance na dukan gidajen Issakar ne, kamar yadda aka rubuta a cikin tarihi, su 87,000 ne duka.

*Zuriyar Benyamin*

6 'Ya'ya uku maza na Benyamin su ne,
Bela, Beker da Yediyayel.
7 'Ya'yan Bela maza su ne,
Ezbon, Uzzi, Uzziyel, Yerimot da Iri, su ne kawunan iyalai, kuma su biyar ne duka. Rubutaccen tarihin zuriyarsu ya nuna suna mazan da sun isa yaƙi 22,034.
8 'Ya'yan Beker maza su ne,
Zemira, Yowash, Eliyezer, Eliyohenai, Omri, Yeremot, Abiya, Anatot da Alemet.
Dukan waɗannan 'ya'yan Beker maza ne. 9 Rubutaccen tarihin zuriyarsu ya
nuna suna da kawunan iyalai da mazan da suka isa yaƙi 20,200.
10 Ɗan Yediyayel shi ne,
Bilhan.
'Ya'yan Bilhan maza su ne,
Yewush, Benyamin, Ehud, Kena'ana, Zetan, Tarshish da Ahishahar. 11 Dukan
waɗannan 'ya'yan Yediyayel maza kawunan iyalai ne. Akwai mazan da suka isa yaƙi waje 17,200.
12 Shuffiyawa da Huffiyawa zuriyar Ir ne, kuma Hushiyawa zuriyar Aher ne.

*Zuriyar Naftali*

13 'Ya'yan Naftali maza su ne,
Yaziyel, Guni, Yezer da Shallum, su zuriyar Bilha ne.

*Zuriyar Manasse*

14 Zuriyar Manasse su ne,

Asriyel zuriyarsa ne ta wurin ƙwarƙwararsa mutuniyar Aram. Ta haifa wa Makir
mahaifin Gileyad. 15 Makir ya auri mata daga cikin Huffiyawa da Shuffiyawa.
'Yar'uwarsa ita ce Ma'aka. Wani daga zuriyar, sunansa Zelofehad, shi yana da
'ya'yan mata ne kawai. 16 Ma'aka matar Makir ta haifi ɗa ta kuma ba shi suna
Feresh. Sunan ɗan'uwansa Sheresh, 'ya'yan Feresh maza kuwa su ne Ulam da Rakem.
17 Ɗan Ulam shi ne,
Bedan.
Duka waɗannan zuriyar Gileyad ne. Gileyad ɗan Makir ne, Makir kuma ɗan Manasse.
18 'Yar'uwarsa Makir mai suna Hammoleket ta haifi Ishod, Abiyezer da Mala.
19 'Ya'yan Shemida maza su ne,
Ahiyan, Shekem, Liki da Aniyam.

### *Zuriyar Efraim*

20 Zuriyar Efraim su ne,
Shutela, Bered,
Tahat, Eleyada,
Tahat 21 Zabad
da Shutela.
Wani ɗan ƙasa haifaffen mutanen Gat ya kashe Ezer da Elad, sa'ad da suka
gangara don su ƙwace dabbobinsu. 22 Mahaifinsu Efraim ya yi makoki dominsu
kwanaki masu yawa sai danginsa suka zo don su yi masa ta'aziyya. 23 Sa'an
nan ya sāke kwana da matarsa, sai ta yi ciki ta haifi ɗa. Ya ba shi suna Beriya,
saboda masifar da ta auko a cikin iyalinsa. 24 'Yarsa ita ce Sheyera, wadda ta
gina Bet-Horon na kwari da na tudu da kuma Uzzen-Sheyera. Zuriyarsa ita ce,
25 Refa, Reshef,
Tela, Tahan,
26 Ladan, Ammihud,
Elishama, 27 Nun
da kuma Yoshuwa.
28 Kasarsu da wuraren zamansu sun haɗa da Betel da ƙauyukan kewayenta,
Na'aran wajen gabas, Gezer da ƙauyukanta wajen yamma, da kuma
Shekem da ƙauyukan da suka nausa har zuwa Aiya da ƙauyukanta. 29 A
iyakokin Manasse akwai Bet-Sheyan, Ta'anak, Megiddo da Dor, tare da
ƙauyukansu. Zuriyar Yusuf ɗan Isra'ila ta zauna a waɗannan garuruwa.

### *Zuriyar Asher*

30 'Ya'yan Asher maza su ne,
Imna, Ishba, Ishwi da Beriya. 'Yar'uwarsa ita ce Sera.
31 'Ya'yan Beriya maza su ne,
Heber da Malkiyel, wanda yake mahaifin Birzayit.
32 Heber shi ne mahaifin Yaflet, Shomer da Hotam da kuma 'yar'uwarsu Shuwa.
33 'Ya'yan Yaflet maza su ne,
Fasak, Bimhal da Ashwat.
Waɗannan su ne 'ya'yan Yaflet maza.
34 'Ya'yan Shemer maza su ne,
Ahi, Roga, Yehubba da Aram.
35 'Ya'yan ɗan'uwansa Helem su ne,
Zofa, Imna, Shelesh da Amal.
36 'Ya'yan Zofa maza su ne,
Suwa, Harnefer, Shuwal, Beri, Imra, 37 Bezer, Hod, Shamma, Shilsha, Itran da Bera.

38 ʼYaʼyan Yeter maza su ne,
Yefunne, Fisfa da Ara.
39 ʼYaʼyan Ulla maza su ne,
Ara, Hanniyel da Riziya.
40 Dukan waɗannan zuriyar Asher ne, kawunan iyalai, zaɓaɓɓun mutane, jarumawa sosai da kuma fitattun shugabanni. Yawan mutanen da suke a shirye don yaƙi, kamar yadda aka lissafta zuriyarsu, 26,000 ne.

# 8

*Zuriyar Shawulu mutumin Benyamin*

1 Benyamin shi ne mahaifin,
Bela ɗansa na fari,
Ashbel ɗansa na biyu, Ahara na uku,
2 Noha na huɗu da Rafa na biyar.
3 ʼYaʼyan Bela maza su ne,
Addar, Gera, Abihud 4 Abishuwa, Naʼaman, Ahowa, 5 Gera, Shefufan da Huram.
6 Waɗannan su ne zuriyar Ehud, waɗanda suke kawunan iyalan waɗanda suke
zama a Geba waɗanda aka kuma kwasa zuwa Manahat.
7 Naʼaman, da Ahiya, da Gera. Gera ne shugabansu lokacin da aka kai su bauta,
shi ne ya haifi Uzza da Ahilud.
8 An haifa ʼyaʼya maza wa Shaharayim a Mowab bayan ya saki matansa Hushim da
Baʼara. 9 Ya haifi Yobab, Zibiya, Hodesh, Malkam, 10 Yewuz, Sakiya da Mirma ta
wurin Hodesh matarsa. Waɗannan su ne ʼyaʼyansa, kawunan iyalai. 11 Ya haifi
Abitub da Efaʼal ta wurin Hushim.
12 ʼYaʼyan Efaʼal maza su ne,
Eber, Misham, Shemed (wanda ya gina Ono da Lod tare da ƙauyukan kewayensu),
13 da Beriya da Shema, waɗanda suke kawunan iyalan waɗanda suke zama a
Aiyalon waɗanda kuma suka kori mazaunan Gat.
14 Ahiyo, Shashak, Yeremot 15 Zebadiya, Arad, Eder, 16 Mikaʼilu, Isfa da Yoha su ne
ʼyaʼyan Beriya maza.
17 Zebadiya, Meshullam, Hizki, Heber, 18 Ishmerai, Izliya da Yobab su ne ʼyaʼyan
Efaʼal maza.
19 Yakim, Zikri, Zabdi, 20 Eliyenai, Zilletai, Eliyel, 21 Adahiya, Berahiya da Shimra su
ne ʼyaʼyan Shimeyi maza.
22 Ishfan, Eber, Eliyel, 23 Abdon, Zikri, Hanan, 24 Hananiya, Elam, Antotiya,
25 Ifdehiya da Fenuwel su ne ʼyaʼyan Shashak maza.
26 Shamsherai, Shehariya, Ataliya, 27 Yaʼareshiya, Iliya da Zikri su ne ʼyaʼyan
Yeroham maza.
28 Dukan waɗannan su ne kawunan iyalai, manya kamar yadda aka lissafta a cikin zuriyarsu, suka zauna a Urushalima.

29 Yehiyel na Gibeyon ya zauna a Gibeyon.
Sunan matarsa Maʼaka, 30 ɗansa na fari kuwa shi ne Abdon, sai Zur, Kish, Baʼal,
Ner, Nadab, 31 Gedor, Ahiyo, Zeker 32 da Miklot, wanda ya zama mahaifin
Shimeya. Su ma sun zauna kusa da danginsu a Urushalima.
33 Ner shi ne mahaifin Kish, Kish mahaifin Shawulu, kuma Shawulu ne mahaifin
Yonatan, Malki-Shuwa, Abinadab da Esh-Baʼal.
34 Ɗan Yonatan shi ne,
Merib-Baʼal* wanda ya zama mahaifin Mika.

* **8:34** Aka kuma sani kamar Mefiboshet

35 ʼYaʼyan Mika maza su ne,
Fiton, Melek, Tereya da Ahaz.
36 Ahaz shi ne mahaifin Yehowadda, Yehowadda shi ne mahaifin Alemet, Azmawet
da Zimri, Zimri kuwa shi ne mahaifin Moza. 37 Moza shi ne mahaifin Bineya;
Rafa, Eleyasa da kuma Azel.
38 Azel yana da ʼyaʼya maza shida, kuma ga sunayensu.
Azrikam, Bokeru, Ishmayel, Sheyariya, Obadiya da Hanan. Dukan waɗannan ʼyaʼyan Azel maza ne.
39 ʼYaʼyan ɗanʼuwansa Eshek su ne,
Ulam ɗan farinsa, Yewush ɗansa na biyu da Elifelet na uku. 40 ʼYaʼyan Ulam
maza jarumawa ne sosai waɗanda suke iya riƙe baka. Suna da ʼyaʼya maza masu yawa da jikoki, 150 gaba ɗaya.
Dukan waɗannan zuriyar Benyamin ne.

# 9

1 Haka aka lissafta dukan Israʼila a tarihin zuriyoyi a littafin sarakunan Israʼila.
Aka kwasa mutanen Yahuda zuwa zaman bauta a Babilon domin rashin aminci.

*Mutanen Urushalima*

2 To, na farkon da aka sāke zaunar da su a mallakarsu a garuruwansu, su ne waɗansu Israʼilawa, firistoci, Lawiyawa da kuma masu hidimar haikali.

3 Waɗanda suke daga Yahuda, daga Benyamin, da kuma daga Efraim da Manasse waɗanda suka zauna a Urushalima su ne,
4 Uttai ɗan Ammihud, ɗan Omri, ɗan Imri, ɗan Bani, zuriyar Ferez ɗan Yahuda.
5 Na mutanen Shilo kuwa su ne,
Asahiya ɗan fari da ʼyaʼyansa maza.
6 Na mutanen Zera su ne,
Yewuyel.
Mutane daga Yahuda sun kai 690.

7 Na Benyamin su ne,
Sallu ɗan Meshullam, ɗan Hodawiya, ɗan Hassenuwa;
8 Ibnehiya ɗan Yeroham;
Ela ɗan Uzzi, ɗan Mikri;
da Meshullam ɗan Shefatiya, ɗan Reyuwel, ɗan Ibniya.
9 Mutane daga Benyamin, kamar yadda aka lissafta zuriyarsu, sun kai 956. Dukan waɗannan mutane kawunan iyalansu ne.

10 Na firistoci su ne,
Yedahiya; Yehoyarib; Yakin;
11 Azariya ɗan Hilkiya, ɗan Meshullam, ɗan Zadok, ɗan Merahiyot, ɗan Ahitub, shugaban da yake lura da gidan Allah;
12 Adahiya ɗan Yeroham, ɗan Fashhur, ɗan Malkiya;
da Maʼasai ɗan Adiyel, ɗan Yazera, ɗan Meshullam, ɗan Meshillemit, ɗan Immer.
13 Firistocin da suke kawunan iyalai, sun kai 1,760. Dukansu ƙwararru ne, masu hakkin hidima a cikin gidan Allah.

14 Na Lawiyawa su ne,
Shemahiya ɗan Hasshub, ɗan Azrikam, ɗan Hashabiya, mutumin Merari;
15 Bakbakkar, Heresh, Galal da Mattaniya ɗan Mika, ɗan Zikri, ɗan Asaf;

16 Obadiya ɗan Shemahiya, ɗan Galal, ɗan Yedutun;
da Berekiya ɗan Asa, ɗan Elkana, wanda ya zauna a ƙauyukan Netofawa.

17 Matsaran ƙofofi su ne,
Shallum, Akkub, Talmon, Ahiman da ʼyanʼuwansu. Shallum ne babbansu 18 da aka ajiye a Kofar Sarki a gabas, har zuwa wannan lokaci. Waɗannan su ne matsaran ƙofofi na sansanin Lawiyawa.
19 Shallum ɗan Kore, ɗan Ebiyasaf, ɗan Kora, da ʼyanʼuwansa matsaran ƙofofi daga iyalin (mutanen Kohat) su suke da hakkin tsaron madogaran ƙofar Tenti kamar dai yadda kakanninsu suka kasance da hakkin tsaron mashigin mazaunin UBANGIJI.
20 A dā Finehas ɗan Eleyazar ne yake lura da matsaran, kuma UBANGIJI ya kasance tare da shi.
21 Zakariya ɗan Meshelemiya shi ne mai tsaro a mashigin Tentin Sujada.
22 Duka-duka, waɗanda aka zaɓa don su zama matsaran madogaran ƙofa sun kai 212. Aka rubuta su zuriya-zuriya a ƙauyukansu.

Dawuda da Samaʼila mai duba ne suka sa matsaran a wurarensu na aminci. 23 Su
da zuriyarsu, su suke lura da tsaron ƙofofin gidan UBANGIJI, gidan da ake kira Tenti.
24 Matsaran suna a kusurwoyi huɗu, gabas, yamma, arewa da kudu. 25 ʼYanʼuwansu a
ƙauyukansu sukan zo lokaci, lokaci su yi ayyukansu kwana bakwai, bakwai. 26 Amma
manyan matsara huɗu, waɗanda suke Lawiyawa, an danƙa musu hakkin lura da
ɗakuna da kuma wuraren ajiya a gidan Allah. 27 Sukan kwana a kewayen gidan
Allah, domin dole su tsare shi; kuma su suke lura da mabuɗi don buɗewa a kowace
safiya.
28 Waɗansunsu su ne suke lura da kayayyakin da ake amfani da su a hidimar
haikali; sukan ƙirga su saʼad da ake shigar da su da saʼad da ake fitar da su. 29 An
sa waɗansu su lura da kayayyakin da kuma dukan waɗansu kayan wuri mai tsarki,
da kuma gari da ruwan inabi, da mai, turare da kuma kayan yaji. 30 Amma waɗansu
firistoci ne suke harhaɗa kayan yajin. 31 Wani Balawe mai suna Mattitiya, ɗan farin
Shallum mutumin Kora ne aka danƙa masa hakkin toya burodin miƙawa. 32 Waɗansu
ʼyanʼuwansu Kohatawa ne suke lura da shiryawa burodin da ake kaiwa a tebur a
kowane Asabbaci.
33 Waɗanda suke mawaƙa, kawunan iyalan Lawiyawa, sukan zauna a ɗakunan
haikali kuma ba sa yin waɗansu ayyuka domin su suke da hakkin aiki dare da rana.
34 Dukan waɗannan su ne kawunan iyalan Lawiyawa, manya kamar yadda aka
lissafta su a zuriyarsu, kuma suna zama a Urushalima.

### *Zuriyar Shawulu*
### *(1 Tarihi 8.29-38)*

35 Yehiyel mahaifin Gibeyon ya zauna a Gibeyon.
Matarsa ita ce Maʼaka 36 ɗansa na fari kuwa shi ne Abdon, sai Zur, Kish, Baʼal,
Ner, Nadab, 37 Gedor, Ahiyo, Zakariya da Miklot. 38 Miklot shi ne mahaifin
Shimeyam. Su ma sun zauna kusa da danginsu a Urushalima.
39 Ner shi mahaifin Kish, Kish mahaifin Shawulu, kuma Shawulu shi ne mahaifin Yonatan, Malki-Shuwa, Abinadab da Esh-Baʼal.*
40 Ɗan Yonatan shi ne,
Merib-Baʼal wanda shi ne mahaifin Mika.
41 ʼYaʼyan Mika maza su ne,
Fiton, Melek, Tareya da Ahaz.

* **9:39** Aka kuma sani da Ish-Boshet

42 Ahaz shi ne mahaifin Yada, Yada shi ne mahaifin Alemet, Azmawet da Zimri,
Zimri kuwa shi ne mahaifin Moza. 43 Moza shi ne mahaifin Bineya; Refahiya,
Eleyasa da kuma Azel.
44 Azel yana da ʼyaʼya maza shida, kuma ga sunayensu.
Azrikam, Bokeru, Ishmayel, Sheyariya, Obadiya da Hanan. Waɗannan su ne ʼyaʼyan Azel maza.

# 10

*Shawulu ya ɗauke ransa*
*(1 Samaʼila 31.1-13)*

1 To, fa, Filistiyawa suka yi yaƙi da Israʼilawa; Israʼilawa kuwa suka gudu a gabansu,
da yawa kuma suka mutu a kan Dutsen Gilbowa. 2 Filistiyawa suka matsa sosai suna
bin Shawulu da ʼyaʼyansa maza, suka kuma kashe ʼyaʼyansa maza Yonatan, Abinadab
da Malki-Shuwa. 3 Yaƙin ya yi tsanani kewaye da Shawulu, kuma saʼad da maharba
suka rutsa shi, sai suka ji masa rauni.
4 Sai Shawulu ya ce wa mai riƙe masa kayan yaƙi, "Zare takobinka ka soke ni, in
ba haka ba waɗannan marasa kaciya za su zo su yi mini baʼa."
Amma mai ɗaukar masa kayan yaƙi ya ji tsoro bai kuwa yi haka ba; saboda haka
Shawulu ya zāre takobinsa ya fāɗi a kansa. 5 Da mai ɗaukar masa kayan yaƙi ya ga
Shawulu ya mutu, sai shi ma ya fāɗi a kan takobinsa ya mutu. 6 Ta haka Shawulu da
ʼyaʼyansa maza uku suka mutu, dukan gidansa kuwa suka mutu tare.
7 Saʼad da dukan Israʼilawa a cikin kwari suka ga cewa mayaƙansu suna gudu,
kuma cewa Shawulu da ʼyaʼyansa maza sun mutu, sai suka bar garuruwansu suka
gudu. Filistiyawa kuwa suka zo suka zauna a cikinsu.
8 Kashegari, da Filistiyawa suka zo don su tuttuɓe waɗanda suka mutu, sai suka
sami Shawulu da ʼyaʼyansa maza sun mutu a Dutsen Gilbowa. 9 Suka tuttuɓe shi suka
yanke kansa suka ɗauka duk da kayan yaƙinsa, suka kuma aika ʼyan aika koʼina a
ƙasar Filistiyawa, a yi shela labarin a cikin gumakansu da kuma mutanensu. 10 Suka
sa kayan yaƙinsa a haikalin allahnsu suka kuma rataye kansa a haikalin Dagon.
11 Saʼad da mazaunan Yabesh Gileyad suka ji dukan abin da Filistiyawa suka yi
wa Shawulu, 12 sai dukan jarumawa suka tafi suka ɗauki jikunan Shawulu da na
ʼyaʼyansa maza suka kawo Yabesh. Saʼan nan suka binne ƙasusuwan a ƙarƙashin
babban itace oak a Yabesh, suka kuma yi azumi kwana bakwai.
13 Shawulu ya mutu domin rashin aminci ga Ubangiji; bai kiyaye maganar Ubangiji
ba, ya ma nemi shawarar mace mai duba, 14 bai kuwa nemi nufin Ubangiji ba. Saboda
haka Ubangiji ya kashe shi, ya miƙa mulkin ga Dawuda ɗan Yesse.

# 11

*Dawuda ya zama sarki a bisa Israʼila*
*(2 Samaʼila 5.1-3)*

1 Dukan Israʼila fa suka taru wurin Dawuda a Hebron suka ce, "Mu jiki da jininka
ne. 2 A dā, ko a lokacin da Shawulu yake sarki, ai, kai ne kake shugabantar Israʼila a
yaƙe-yaƙe. Kuma Ubangiji Allahnka ya ce maka, ʻZa ka zama makiyayin mutanena
Israʼila, za ka kuma zama mai mulkinsu.ʼ "
3 Saʼad da dukan dattawan Israʼila suka zo wurin Sarki Dawuda a Hebron, suka yi
yarjejjeniya da shi a gaban Ubangiji, suka kuwa shafe Dawuda ya zama sarki a bisa
Israʼila, yadda Ubangiji ya yi alkawari ta wurin Samaʼila.

*Dawuda ya ci Urushalima*
*(2 Samaʼila 5.6-10)*

[4] Dawuda tare da dukan Isra'ilawa suka taka zuwa Urushalima (wato, Yebus).
Yebusiyawan da suke zama a wurin [5] suka ce wa Dawuda, "Ba za ka shiga nan ba."
Duk da haka, Dawuda ya ci kagarar Sihiyona, Birnin Dawuda.

[6] Dawuda ya ce, "Duk wanda ya jagoranci yaƙi a kan Yebusiyawa zai zama babban shugaban mayaƙa." Yowab ɗan Zeruhiya ya fara haurawa, ta haka ya zama shugaba.

[7] Dawuda zauna a kagarar, ta haka aka kira ta Birnin Dawuda. [8] Sai ya gina birni
kewaye da shi, daga madogaran gini zuwa katangar da take kewaye, yayinda Yowab
ya maido da sauran birnin. [9] Dawuda kuwa ya ƙara ƙarfi, domin UBANGIJI Maɗaukaki
yana tare da shi.

*Jarumawan Dawuda*
*(2 Sama'ila 23.8-17)*

[10] Waɗannan su ne manyan jarumawan Dawuda, su ne, tare da dukan Isra'ila, suka
ba wa mulkinsa goyon baya mai ƙarfi da ya kai bisa dukan ƙasar, yadda UBANGIJI ya
yi alkawari. [11] Ga jerin sunayen jarumawan Dawuda.

Yashobeyam wani ɗan Hakmoni, shi ne babban shugaba; ya ɗaga māshinsa a kan mutum ɗari uku, waɗanda ya kashe a ƙarawa guda kawai.

[12] Biye da shi, shi ne Eleyazar ɗan Dodo mutumin Aho, ɗaya daga cikin jarumawa
uku. [13] Yana tare da Dawuda a Fas Dammim sa'ad da Filistiyawa suka taru can don
yaƙi. A wani wuri inda akwai gona cike da sha'ir, sojoji suka gudu daga Filistiyawa.
[14] Sai shi da Dawuda suka shiga gonar sha'ir ɗin, suka tsaya ciki don su tsare ta. Suka
ragargaza Filistiyawa, UBANGIJI kuma ya kawo babban nasara.

[15] Wata rana uku cikin manyan mutanen nan talatin suka gangara wurin Dawuda
zuwa dutse a kogon Adullam, yayinda ƙungiyar Filistiyawa suke sansani a Kwarin
Refayim. [16] A lokacin Dawuda yana cikin mafaka, sojojin Filistiyawa kuma suna a
Betlehem. [17] Dawuda ya ji marmarin ruwan sha sai ya ce, "Kash, a ce wani zai sami
mini ruwan sha daga rijiya kusa da ƙofar Betlehem mana!" [18] Sai Ukun suka kutsa kai
cikin sansanin Filistiyawa, suka ja ruwa daga rijiyar da take kusa da ƙofar Betlehem
suka ɗauko shi suka kawo wa Dawuda. Amma ya ƙi yǎ sha; a maimako, sai ya zubar
da shi a gaban UBANGIJI. [19] Ya ce, "Allah yǎ sawwaƙe in yi haka, ya kamata in sha
jinin waɗannan mutanen da suka yi kasai da rayukansu?" Domin sun yi kasai da
rayukansu don su dawo da shi, Dawuda bai sha shi ba.

Irin abubuwan da jarumawa ukun nan suka yi ke nan.

*(2 Sama'ila 23.18-39)*

[20] Abishai ɗan'uwan Yowab shi ma babba ne cikin Ukun nan. Ya ɗaga māshinsa
a kan mutum ɗari uku, waɗanda ya kashe, ya kuma zama sananne kamar Ukun.
[21] Aka ninka girmama shi bisa Ukun, sai ya zama shugaba, ko da yake ba a haɗa shi
a cikinsu ba.

[22] Benahiya ɗan Yehohiyada shi ma wani barden yaƙi ne daga Kabzeyel, wanda
ya yi manyan abubuwa. Ya bugi gwanayen Mowab biyu. Ya kuma gangara zuwa
cikin rami a ranar da aka yi dusar ƙanƙara ya kashe zaki. [23] Ya kuma kashe wani
mutumin Masar mai tsayi ƙafa bakwai da rabi. Ko da yake mutumin Masar yana
da māshi kamar sandan masaƙa a hannunsa, Benahiya ya yaƙe shi da kulki. Ya
ƙwace māshin daga hannun mutumin Masar ya kuma kashe shi da māshin nan
nasa. [24] Irin abubuwan da Benahiya ɗan Yehohiyada ya yi ke nan; shi ma sananne
ne kamar waɗannan jarumawa uku. [25] Aka ɗauka shi da bangirma fiye da Talatin
nan, amma ba a haɗa shi cikin Ukun ba. Dawuda kuwa ya sa shi yǎ lura da masu
tsaron lafiyarsa.

[26] Jarumawan nan su ne,

Asahel ɗan'uwan Yowab,
Elhanan ɗan Dodo daga Betlehem,
27 Shammot mutumin Haror,
Helez mutumin Felon,
28 Ira ɗan Ikkesh daga Tekowa,
Abiyezer daga Anatot,
29 Sibbekai mutumin Husha,
Ilai mutumin Aho,
30 Maharai mutumin Netofa,
Heled ɗan Ba'ana mutumin Netofa,
31 Ittai ɗan Ribai daga Gibeya a Benyamin,
Benahiya mutumin Firaton,
32 Hurai daga kogunan Ga'ash,
Abiyel mutumin Arba,
33 Azmawet mutumin Harum,
Eliyaba mutumin Sha'albo,
34 'ya'yan Hashem mutumin Gizon maza,
Yonatan ɗan Shageye mutumin Harar,
35 Ahiyam ɗan Sakar mutumin Harar,
Elifal ɗan Ur,
36 Hefer mutumin Mekerat,
Ahiya mutumin Felon,
37 Hezro mutumin Karmel,
Na'arai ɗan Ezbai,
38 Yowel ɗan'uwan Natan,
Mibhar ɗan Hagiri,
39 Zelek mutumin Ammon
Naharai Baroti, mai ɗaukar kayan yaƙin Yowab ɗan Zeruhiya,
40 Ira mutumin Itra,
Gareb mutumin Itra,
41 Uriya mutumin Hitti
Zabad ɗan Alai,
42 Adina ɗan Shiza mutumin Ruben, wanda shi ne babba na mutanen Ruben, kuma talatin suna tare da shi,
43 Hanan ɗan Ma'aka,
Yoshafat mutumin Mit,
44 Uzziya mutumin Ashtarot,
Shama da Yehiyel 'ya'yan Hotam mutumin Arower maza,
45 Yediyayel ɗan Shimri,
ɗan'uwansa Yoha mutumin Tiz,
46 Eliyel mutumin Ma'aha,
Yeribai da Yoshawiya 'ya'yan Elna'am maza,
Itma mutumin Mowab,
47 Eliyel, Obed da Ya'asiyel mutumin Mezob.

# 12

### *Jarumawa sun haɗa kai da Dawuda*

1 Waɗannan su ne mutanen da suka zo wurin Dawuda a Ziklag, yayinda
aka kore shi daga gaban Shawulu ɗan Kish (suna cikin jarumawan da
suka taimake shi a yaƙi; 2 suna da baka suna kuma iya harba kibiya, ko

majajjawa da hannun dama ko na hagu; su ʼyanʼuwan Shawulu ne daga kabilar Benyamin):

3 Ahiyezer babbansu da Yowash ʼyaʼyan Shemaʼa maza daga Gibeya;
Yeziyel da Felet ʼyaʼyan Azmawet;
Beraka, Yehu daga Anatot, 4 da Ishmahiya daga Gibeyon, wani jarumi a cikin Talatin nan, wanda shi ne shugaban Talatin;
Irmiya, Yahaziyel, Yohanan, Yozabad daga Gedera, 5 Eluzai, Yerimot, Beyaliya, Shemariya da Shefatiya daga Haruf;
6 Elkana, Isshiya, Azarel, Yoyezer da Yashobeyam daga Kora;
7 da Yoyela da Zebadiya ʼyaʼyan Yeroham maza daga Gedor.

8 Sai waɗansu mutanen Gad suka koma suna goyon bayan Dawuda suka kuma
haɗa kai da shi a kagararsa a hamada. Su ƙwararrun mayaƙa ne, a shirye don yaƙi,
kuma suna iya riƙe garkuwa da māshi. Fuskokinsu kamar fuskoki zakoki, kuma suna
da sauri kamar bareyi a kan duwatsu.

9 Ezer shi ne babba,
Obadiya shi ne mai binsa a shugabanci, Eliyab na uku,
10 Mismanna na huɗu, Irmiya na biyar,
11 Attai na shida, Eliyel na bakwai,
12 Yohanan na takwas, Elzabad na tara,
13 Irmiya na goma da kuma Makbannai na goma sha ɗaya.

14 Waɗannan mutanen Gad shugabannin mayaƙa ne; ƙarami a cikinsu zai iya ƙara
da mutum ɗari, kuma babba a cikin zai iya ƙara da dubu. 15 Su ne suka haye Urdun
a wata na farko saʼad da kogin ya yi ambaliya, suka kuma kori duk mai rai a kwarin,
na wajen gabas da na wajen yamma.
16 Sauran mutanen Benyamin da waɗansu mutanen Yahuda su ma suka zo wurin
Dawuda a kagararsa. 17 Sai Dawuda ya fita don yă tarye su, ya kuma ce musu, “In
kun zo wurina da salama, don ku taimake ni, to, ina a shirye in bar ku ku haɗa kai
tare da ni. Amma in kun zo don ku bashe ni ga abokan gābana saʼad da hannuwana
ba su da laifi a rikici, bari Allah na kakanninmu yă duba yă kuma shariʼanta ku.”
18 Sai Ruhu ya sauko a kan Amasai, shugaban Talatin nan, sai ya ce,
“Mu naka ne, ya Dawuda!
Muna tare da kai, ya ɗan Yesse!
Nasara, nasara gare ka,
nasara kuma ga waɗanda suke taimakonka.
Gama Allahnka zai taimake ka.”
Saboda haka Dawuda ya karɓe su ya kuma mai da su shugabannin ƙungiyoyin maharansa.
19 Waɗansu mutanen Manasse suka haɗa kai da Dawuda saʼad da ya tafi tare da
Filistiyawa don yă yaƙi Shawulu (Shi da mutanensa ba su taimaki Filistiyawa ba
domin bayan shawarwari, shugabanninsu suka salame shi. Sun ce, “Za mu biya
da kawunanmu in ya koma ga maigidansa Shawulu.”) 20 Da Dawuda ya tafi Ziklag,
waɗannan mutanen Manasse ne suka haɗa kai da shi. Adna, Yozabad, Yediyayel,
Mikaʼilu, Yozabad, Elihu da Zilletai, shugabannin ƙungiyoyi na dubu a cikin Manasse.
21 Suka taimaki Dawuda a kan ƙungiyoyin hari, gama dukansu jarumawa ne sosai,
kuma su shugabanni ne a cikin mayaƙansa. 22 Kowace rana mutane suka riƙa zuwa
don su taimaki Dawuda, sai da ya kasance da runduna mai girma, kamar mayaƙan
Allah.

### *Saura sun haɗa kai da Dawuda a Hebron*

23 Ga yawan mutanen shiryayyu don yaƙi waɗanda suka zo wurin Dawuda a Hebron don su mai da mulkin Shawulu gare shi, yadda UBANGIJI ya faɗa.

24 Mutanen Yahuda, masu riƙe garkuwa da māshi, su 6,800 shiryayyu don yaƙi;
25 mutanen Simeyon, jarumawa shiryayyu don yaƙi, su 7,100;
26 mutanen Lawi, su 4,600, 27 haɗe da Yehohiyada, shugaban iyalin Haruna tare da mutane 3,700, 28 da Zadok, matashi jarumi sosai, tare da shugabanni su 22 daga iyalinsa;
29 mutanen Benyamin, ’yan’uwan Shawulu, su 3,000, yawanci waɗanda suke biyayya ga gidan Shawulu sai lokacin;
30 mutanen Efraim, jarumawa, sanannu cikin gidajensu, su 20 800;
31 mutanen rabin kabilar Manasse, sanannu da sunaye suka zo suka mai da Dawuda sarki, su 18,000;
32 mutanen Issakar, masu fahimtar lokuta suka kuma san abin da ya kamata Isra’ila ya yi, manya 200, tare da danginsu a ƙarƙashin shugabancinsu;
33 mutanen Zebulun, ƙwvararru sojoji shiryayyu don yaƙi da kowane irin makami, suka zo don su taimaki Dawuda da zuciya ɗaya, su 50,000;
34 mutanen Naftali su 1,000 shugabanni, tare da mutane 37,000 masu riƙe garkuwa da masu;
35 mutanen Dan, shiryayyu don yaƙi, su 28,600;
36 mutanen Asher, ƙwararrun sojoji shiryayyu don yaƙi, su 40,000;
37 kuma daga gabashin Urdun, mutanen Ruben, Gad da kuma rabin kabilar Manasse, masu kayan yaƙi iri-iri, su 120,000.

38 Dukan waɗannan mayaƙa ne waɗanda suka ba da kansu da yardar rai su yi hidima.

Suka zo Hebron da cikakken niyya don su naɗa Dawuda sarki a bisa dukan Isra’ila.
Duka sauran Isra’ilawa su ma suka goyi baya a naɗa Dawuda sarki. 39 Mutanen suka
yi kwana uku a can tare da Dawuda, suna ci suna sha, gama iyalansu sun yi musu
tanadi. 40 Haka ma, maƙwabtansu daga nesa har Issakar, Zebulun da Naftali suka
zo suka kawo abinci a kan jakuna, raƙuma, alfadarai da shanu. Akwai tanadin mai
yawa na gari, kauɗar ɓaure, nonnan busassun ’ya’yan inabi, ruwan inabi, mai, shanu
da tumaki. Duk an yi haka don a nuna farin ciki ƙwarai a cikin dukan ƙasar Isra’ila.

# 13

### *Dawowa da akwatin alkawari*
### *(2 Sama’ila 6.1-12)*

1 Sai Dawuda ya tattauna da kowane ɗaya daga cikin shugabanninsa, shugabannin
sojoji na dubu-dubu da na ɗari-ɗari. 2 Sa’an nan ya ce wa dukan taron Isra’ila, “In
ya yi muku kyau kuma in nufin UBANGIJI Allahnmu ne, bari mu aika da saƙo nesa da
kuma ko’ina zuwa ga sauran ’yan’uwanmu a duk iyakokin Isra’ila, da kuma zuwa
ga firistoci da Lawiyawa waɗanda suke tare da su a garuruwansu da makiyayansu,
su zo wurinmu. 3 Bari mu ɗauko akwatin alkawarin Allahnmu mu kawo wurinmu,
gama ba mu neme shi a lokacin mulkin Shawulu ba.” 4 Dukan taron jama’a suka
yarda su yi haka, domin ya yi daidai ga dukan mutane.
5 Saboda haka Dawuda ya tattara dukan Isra’ilawa, daga Kogin Shihor a Masar zuwa
Lebo Hamat, don su kawo akwatin alkawarin Allah daga Kiriyat Yeyarim. 6 Dawuda
da dukan Isra’ilawa tare da shi suka tafi Ba’ala na Yahuda (Kiriyat Yeyarim) don

su haura daga can su kawo akwatin alkawarin Allah Ubangiji, wanda yake zama tsakanin kerubobi, akwatin alkawarin da ake kira da Sunan.

7 Suka ɗauki akwatin alkawarin Allah daga gidan Abinadab a kan sabon keken shanu, Uzza da Ahiyo ne suke lura da shi. 8 Dawuda da dukan Isra'ilawa suka yi shagali da dukan ƙarfinsu a gaban Allah, tare da waƙoƙi da garayu, molaye, ganguna, kuge da ƙahoni.

9 Sa'ad da suka kai masussukar Kidon, Uzza ya miƙa hannunsa don yă gyara akwatin alkawarin, gama shanun sun yi tuntuɓe. 10 Sai fushin Ubangiji ya ƙuna a kan Uzza, ya kuma buge shi domin ya sa hannunsa a kan akwatin alkawarin. Sai ya mutu a can a gaban Allah.

11 Ran Dawuda ya ɓace domin Ubangiji ya husata a kan Uzza, kuma har wa yau ana ce da wannan wuri Ferez Uzza.*

12 Dawuda ya ji tsoron Allah a wannan rana ya kuma yi tambaya, "Yaya zan taɓa kawo akwatin alkawarin Allah gare ni?" 13 Don haka bai ɗauki akwatin alkawarin ya kasance tare da shi a Birnin Dawuda ba. A maimakon haka, ya kai shi gidan Obed-Edom mutumin Gat. 14 Akwatin Alkawarin Allah ya zauna tare da iyalin Obed-Edom a gidansa wata uku, Ubangiji kuwa ya albarkaci gidan Obed-Edom da kome da yake da shi.

# 14

### *Gida da iyalin Dawuda*
### *(2 Sama'ila 5.11-16)*

1 To, fa, Hiram sarkin Taya ya aika da 'yan aika zuwa wurin Dawuda, tare da gumaguman al'ul, maginan duwatsu da kafintoci, don su gina wa Dawuda fada. 2 Dawuda kuwa ya san cewa Ubangiji ya kafa shi a matsayin sarki a bisa Isra'ila kuma cewa an ɗaukaka mulkinsa saboda mutanensa Isra'ila.

3 A Urushalima, Dawuda ya ƙara auren waɗansu mata, ya kuma zama mahaifin ƙarin 'ya'yan maza da mata. 4 Ga sunayen yaran da aka haifa masa a can. Shammuwa, Shobab, Natan, Solomon, 5 Ibhar, Elishuwa, Elfelet, 6 Noga, Nefeg, Yafiya, 7 Elishama, Beyeliyada da Elifelet.

### *Dawuda ya ci Filistiyawa da yaƙi*
### *(2 Sama'ila 5.17-25)*

8 Sa'ad da Filistiyawa suka ji an naɗa Dawuda sarki a bisa dukan Isra'ila, sai suka haura da cikakken mayaƙa don su neme shi, amma Dawuda ya ji game da wannan ya kuwa fita don yă ƙara da su. 9 To, fa, Filistiyawa suka zo suka kai wa Kwarin Refayim hari; 10 sai Dawuda ya roƙi Allah ya ce, "In tafi in yaƙi Filistiyawa? Za ka ba da su gare ni?"

Ubangiji ya amsa masa ya ce, "Ka tafi, zan ba da su gare ka."

11 Saboda haka Dawuda da mutanensa suka haura zuwa Ba'al-Ferazim, a can kuwa suka ci Filistiyawa da yaƙi. Sai ya ce, "Kamar yadda ruwa kan raraki ƙasa, haka Allah ya raraki abokan gābana ta wurin hannuna." Saboda haka aka kira wurin Ba'al-Ferazim. 12 Filistiyawa suka yashe allolinsu, Dawuda kuma ya ba da umarnai a ƙone su a wuta.

13 Filistiyawa suka sāke kai hari wa kwarin; 14 sai Dawuda ya sāke roƙi Allah, Allah kuwa ya amsa masa, "Kada ka tafi kai tsaye, amma ka yi zobe kewaye da su, ka kuma fāɗa musu a gaban itatuwan tsamiya. 15 Da zarar ka ji motsin takawa a sama itatuwan tsamiya, ka fita don yaƙi, domin wannan zai nuna cewa Allah ya fita a gabanka don yă bugi mayaƙan Filistiyawa." 16 Saboda haka Dawuda ya yi kamar

---

* **13:11** Ferez Uzza yana nufin hasala a kan Uzza.

yadda Allah ya umarce shi, suka kuma bugi mayaƙan Filistiyawa, tun daga Gibeyon har zuwa Gezer.
17 Sai sunan Dawuda ya bazu koʼina a ƙasar, UBANGIJI kuwa ya sa dukan alʼummai suka ji tsoronsa.

# 15

*An kawo akwatin alkawari a Urushalima*

1 Bayan Dawuda ya yi gine-gine wa kansa a Birnin Dawuda, sai ya shirya wuri
domin akwatin alkawarin Allah, ya kuma kafa tenti dominsa. 2 Saʼan nan Dawuda
ya ce, "Babu wani sai ko Lawiyawa kaɗai za su ɗauka akwatin alkawarin Allah,
gama UBANGIJI ya zaɓe su su ɗauka akwatin alkawarin UBANGIJI su kuma yi hidima
a gabansa har abada."
3 Dawuda ya tattara dukan Israʼila a Urushalima don su haura da akwatin
alkawarin UBANGIJI zuwa wurin da aka shirya dominsa.

4 Ya tattara zuriyar Haruna a wuri ɗaya da kuma Lawiyawa.

5 Daga zuriyar Kohat,
Uriyel shugaba da dangi 120;
6 daga zuriyar Merari
Asahiya shugaba da dangi 220;
7 daga zuriyar Gershom,
Yowel shugaba da dangi 130;
8 daga zuriyar Elizafan,
Shemahiya shugaba da dangi 200;
9 daga zuriyar Hebron,
Eliyel shugaba da dangi 80;
10 daga zuriyar Uzziyel,
Amminadab shugaba da dangi 112.

11 Saʼan nan Dawuda ya kira Zadok da Abiyatar, firistoci, tare da Uriyel, Asahiya,
Yowel, Shemahiya, Eliyel da Amminadab, Lawiyawa. 12 Ya ce musu, "Ku ne kawunan
iyalan Lawiyawa; ku da ʼyanʼuwanku Lawiyawa, sai ku tsarkake kanku ku hauro
da akwatin alkawarin UBANGIJI, Allah na Israʼila, zuwa wurin da na shirya dominsa.
13 Domin ku, Lawiyawa ba ku haura da shi da farko ba ne ya sa UBANGIJI Allahnmu
ya husata a kanmu. Ba mu tambaye shi game da yadda za mu yi shi a hanyar da
aka ƙayyade ba." 14 Saboda haka firistoci da Lawiyawa suka tsarkake kansu don su
hauro da akwatin alkawarin UBANGIJI, Allah na Israʼila. 15 Sai Lawiyawa suka ɗauki
akwatin alkawarin Allah da sanduna a kafaɗunsu, kamar yadda Musa ya umarta bisa
ga maganar UBANGIJI.
16 Dawuda ya faɗa wa shugabannin Lawiyawa su sa ʼyanʼuwansu su zama mawaƙa
don su rera waƙoƙi masu farin ciki, da kayayyakin bushe-bushe, da kaɗe-kaɗe,
molaye, garayu da ganguna.
17 Saboda haka Lawiyawa suka zaɓi Heman ɗan Yowel, da Asaf ɗan Berekiya daga
cikin ʼyanʼuwansu. Daga iyalin Merari kuma aka zaɓi Etan ɗan Kushahiya. 18 Tare
da su kuma ʼyanʼuwansa da suke biye bisa ga matsayi. Wato, Zakariya,* Yaʼaziyel,

* **15:18** Rubuce-rubucen Ibraniyanci guda uku da kuma yawancin rubuce-rubucen Seftuwajin (duba kuma aya 20 da 1Tar 16.5); yawancin Rubuce-rubucen Ibraniyanci Zakariya ɗan da kuma ko Zakariya, Ben da

Shemiramot, Yehiyel, Unni, Eliyab, Ben, Ma'asehiya, Mattitiya, Elifelehu, Miknehiya,
Obed-Edom da Yehiyel,† matsaran ƙofofi.
19 Mawaƙan nan Heman, Asaf da Etan, ne za su buga kugen tagulla. 20 Zakariya,
Aziyel, Shemiramot, Yehiyel, Unni, Eliyab, Ma'asehiya da Benahiya, ne za su kaɗa
molaye masu murya sama-sama, bisa ga *alamot.* 21 Mattitiya, Elifelehu, Miknehiya,
Obed-Edom, Yehiyel da Azaziya, ne za su ja garayu masu murya ƙasa-ƙasa bisa
ga *sheminit.* 22 Kenaniya, shugaban Lawiyawa, shi ne mai bi da waƙoƙi. Wannan
hakkinsa ne, gama shi gwani ne a wannan fanni.
23 Berekiya da Elkana, ne za su zama masu lura da ƙofofi domin akwatin alkawarin.
24 Shebaniya, Yoshafat, Netanel, Amasai, Zakariya, Benahiya da Eliyezer firistoci, su
ne za su busa ƙahoni a gaban akwatin alkawarin Allah. Obed-Edom da Yehiya su ma
za su zama masu lura da ƙofofi domin akwatin alkawarin.

*(2 Sama'ila 6.12-22)*

25 Sai Dawuda da dattawan Isra'ila da shugabannin ƙungiyoyi dubu suka haura
don su kawo akwatin alkawarin UBANGIJI daga gidan Obed-Edom, da farin ciki.
26 Domin Allah ya taimaki Lawiyawan da suke ɗaukar akwatin alkawarin UBANGIJI,
aka miƙa hadayar bijimai bakwai da raguna bakwai. 27 To, fa, Dawuda yana saye da
kyakkyawar rigar lilin, kamar yadda dukan Lawiyawa waɗanda suke ɗaukar akwatin
alkawarin suka sa, da kuma yadda mawaƙa, da Kenaniya, wanda yake bi da waƙar
mawaƙan ya sa. Dawuda kuma ya sa efod lilin. 28 Sai dukan Isra'ila suka kawo
akwatin alkawarin UBANGIJI da sowa, da ƙarar ƙahonin raguna da busan ƙahoni, da
na ganguna, suna kuma kaɗa molaye da garayu.
29 Yayinda akwatin alkawarin UBANGIJI yake shiga Birnin Dawuda, Mikal 'yar
Shawulu ta leƙa daga taga. Sa'ad da ta ga Sarki Dawuda yana rawa yana shagali,
sai ta rena masa wayo a zuciyarta.

# 16

*Yin hidima a gaban akwatin alkawari*

1 Suka fa kawo akwatin alkawarin Allah, suka sa a cikin tentin da Dawuda ya kafa
dominsa, suka kuma miƙa hadayun ƙonawa da hadayu na salama a gaban Allah.
2 Bayan Dawuda ya gama miƙa hadayu na ƙonawa da hadayu na salama, sai ya
albarkaci mutane a cikin sunan UBANGIJI. 3 Sa'an nan ya ba da dunƙulen burodi
da wainar dabino da kuma kauɗar zabibi ga kowane mutumin Isra'ila namiji da ta
mace.
4 Ya sa Lawiyawa su yi hidima a gaban akwatin alkawarin UBANGIJI, su ɗaukaka,
su gode, su kuma yabi UBANGIJI, Allah na Isra'ila. 5 Asaf shi ne babba, sai Zakariya
na biye, sa'an nan Ya'aziyel, Shemiramot, Yehiyel, Mattitiya, Eliyab, Benahiya, Obed-
Edom da Yehiyel. Su ne za su kaɗa molaye, da garayu, Asaf kuwa zai buga ganguna,
6 Benahiya da Yahaziyel firistoci za su busa ƙahoni kullum a gaban akwatin alkawarin
Allah.

*Zaburar Dawuda ta godiya*
*(Zabura 105.1-15; 96.1-13; 106.1,47,48)*

7 A wannan rana, da farko, Dawuda ya sa Asaf da 'yan'uwansa su rera wannan
zabura ta yabo ga UBANGIJI.
8 Ku yi godiya ga UBANGIJI, ku yi shelar sunansa;
ku sanar a cikin al'ummai abin da ya yi.
9 Ku rera gare shi, ku rera yabo gare shi;
ku faɗa dukan ayyukan banmamakinsa.

† **15:18** Da Ibraniyanci; Seftuwajin (duba kuma aya 21) Yehiyel da Azaziya

10 Ku ɗaukaka a cikin sunansa mai tsarki
bari zukatan waɗanda suke neman UBANGIJI su yi farin ciki.
11 Ku dogara ga UBANGIJI da kuma ƙarfinsa;
ku nemi fuskarsa kullum.

12 Ku tuna ayyukan banmamakin da ya aikata,
mu'ujizansa da kuma hukuntai da ya yanke,
13 Ya ku zuriyar Isra'ila bayinsa,
Ya ku 'ya'yan Yaƙub maza, zaɓaɓɓunsa.
14 Shi ne UBANGIJI Allahnmu;
hukuntansa suna a cikin dukan duniya.

15 Yakan tuna da alkawarinsa har abada,
maganar da ya umarta, har tsararraki dubu,
16 alkawarin da ya yi wa Ibrahim
rantsuwar da ya yi ga Ishaku.
17 Ya tabbatar da shi ga Yaƙub kamar ƙa'ida,
ga Isra'ila kamar madawwamin alkawari.
18 "Gare ka zan ba da ƙasar Kan'ana
kamar rabon da za ka gāda."

19 Sa'ad da suke kima,
kima sosai, da kuma baƙi a cikinta,
20 suka yi ta yawo daga al'umma zuwa al'umma,
daga wannan mulki zuwa wancan.
21 Bai bar wani ya zalunce su ba;
saboda su ya tsawata wa sarakuna.
22 "Kada ku taɓa shafaffuna;
kada ku yi wa annabawana lahani."

23 Ku rera ga UBANGIJI, ku duniya duka;
ku yi shelar cetonsa kowace rana.
24 Ku furta ɗaukakarsa a cikin al'ummai,
ayyukansa masu al'ajabai a cikin mutane.

25 Gama UBANGIJI mai girma ne ya kuma cancanci yabo;
dole a ji tsoronsa fiye da dukan alloli.
26 Gama dukan allolin al'ummai gumaka ne,
amma UBANGIJI ya yi sammai.
27 Daraja da ɗaukaka suna a gabansa;
ƙarfi da farin ciki suna a wurin zamansa.

28 Ku yabi UBANGIJI, ku iyalan al'ummai,
ku yabi ɗaukaka da ƙarfin UBANGIJI,
29 ku ba wa UBANGIJI ɗaukakar da ta dace da sunansa.
Ku kawo hadaya ku kuma zo gabansa;
ku yi wa UBANGIJI sujada cikin darajar tsarkinsa.
30 Ku yi rawar jiki a gabansa, ya ku duniya duka!
Duniya ta kahu sosai; ba za tă jijjigu ba.

31 Bari sammai su yi farin ciki, bari duniya tă yi murna;

bari su ce a cikin al'ummai, "UBANGIJI yana mulki!"
32 Bari teku da kome da yake cikinsa su yi ruri;
bari gonaki da kome a cikinsu su yi farin ciki!
33 Sa'an nan itatuwan jeji za su rera,
za su rera don farin ciki a gaban UBANGIJI,
gama ya zo don yǎ hukunta duniya.

34 Ku yi godiya ga UBANGIJI, gama shi nagari ne;
ƙaunarsa madawwamiya ce.
35 Ku yi kuka, ku ce, "Cece mu, ya Allah Mai Cetonmu;
tara mu ka kuma cece mu daga al'ummai,
don mu yi godiya ga sunanka mai tsarki,
don mu ɗaukaka a cikin yabonka."
36 Yabi UBANGIJI, Allah na Isra'ila,
daga madawwami zuwa madawwami.
Sai dukan mutane suka ce, "Amin." Suka kuma "Yabi UBANGIJI."

37 Dawuda ya bar Asaf da 'yan'uwansa a gaban akwatin alkawarin UBANGIJI don
su yi hidima a can kullum, bisa ga tsari na kowace rana. 38 Ya kuma bar Obed-Edom
da 'yan'uwansa sittin da takwas don su yi hidima tare. Obed-Edom ɗan Yedutun da
Hosa kuma, su ne matsaran ƙofofi.
39 Dawuda ya bar Zadok firist da 'yan'uwansa firistoci a gaban tabanakul na
UBANGIJI a tudun da yake a Gibeyon 40 don su miƙa hadayun ƙonawa ga UBANGIJI
a kan bagaden hadaya ta ƙonawa kullum, da safe da kuma yamma, bisa ga kome da
yake a rubutacce a cikin Dokar UBANGIJI, da ya ba wa Isra'ila. 41 Tare da su akwai
Heman da Yedutun da sauran waɗannan zaɓaɓɓun da aka rubuta sunansu don yin
godiya ga UBANGIJI, "gama ƙaunarsa madawwamiya ce har abada." 42 Heman da
Yedutun su ne da hakkin busa ƙahoni da kaɗa kuge da sauran kayan bushe-bushe da
na kaɗe-kaɗe, waɗanda ake amfani da su lokacin da ake rera waƙoƙi masu tsarki.
'Ya'yan Yedutun maza, su aka ba wa aikin tsaron ƙofa.
43 Sa'an nan dukan mutanen suka tashi, kowa ya koma gidansa, Dawuda ya koma
gida yǎ sa wa iyalinsa albarka.

# 17

*Alkawarin Allah ga Dawuda*
*(2 Sama'ila 7.1-17)*

1 Bayan Dawuda ya zauna a fadansa, sai ya ce wa annabi Natan, "Ga ni, ina zama a
fadar da aka yi da al'ul, yayinda akwatin alkawarin UBANGIJI yana a ƙarƙashin tenti."
2 Natan ya amsa wa Dawuda ya ce, "Duk abin da kake tunani a zuciya, ka yi, gama
Allah yana tare da kai."
3 A daren nan maganar Allah ta zo wa Natan cewa,
4 "Ka tafi ka faɗa wa bawana Dawuda, 'Ga abin da UBANGIJI ya ce ba kai ba ne
za ka gida mini gidan da zan zauna a ciki. 5 Ban taɓa zama a gida daga ranar da
na fito da Isra'ila daga Masar ba har wa yau. Na yi ta yawo daga gefen da aka
kafa tenti zuwa wani, daga wannan wuri zuwa wancan. 6 Duk inda na tafi tare da
Isra'ilawa, na taɓa ce wa wani daga cikin shugabanninsu waɗanda na umarta su
yi kiwon mutanena, "Don me ba ku gida mini gidan al'ul ba?" '
7 "Yanzu, ka faɗa wa bawana Dawuda, 'Ga abin da UBANGIJI Maɗaukaki ya ce, na
ɗauke ka daga makiyaya da kuma daga bin garke, don ka zama mai mulki a bisa
mutanena Isra'ila. 8 Na kasance tare da kai ko'ina ka tafi, na kuma yanke dukan

abokan gābanka a gabanka. Yanzu zan sa sunanka kamar sunayen mutane mafi
girma na duniya. 9 Zan kuma tanada wuri domin mutanena Isra'ila, zan kuma kafa
su saboda za su kasance da gidan kansu ba kuwa za a ƙara damunsu ba. Mugayen
mutane ba za su ƙara zaluntar su ba, yadda suka yi da farko 10 da kuma suka yi tun
lokacin da na sa shugabanni a bisa mutanen Isra'ila. Zan rinjaye dukan abokan
gābanka.
" 'Na furta maka cewa Ubangiji zai gina maka gida, 11 sa'ad da kwanakinka suka
ƙare ka kuma tafi don ka kasance da kakanninka, zan tā da ɗaya cikin 'ya'yanka
maza, daga zuriyarka yă gāje ka, zan kuma kafa mulkinka. 12 Shi ne zai gina gida
domina, zan kuma kafa sarautarsa har abada. 13 Zan zama Ubansa, zai kuma zama
ɗana. Ba zan taɓa ɗauke ƙaunata daga gare shi, kamar yadda na ɗauke ta daga
wanda ya riga ka ba. 14 Zan sa shi a bisa gidana da mulkina har abada; kujerar
sarautarsa za tă kahu har abada.' "
15 Natan ya faɗa wa Dawuda dukan kalmomin wahayin nan.

### *Addu'ar Dawuda*
### *(2 Sama'ila 7.18-29)*

16 Sai Sarki Dawuda ya shiga ya zauna a gaban Ubangiji ya ce,
"Wane ne ni, ya Ubangiji Allah, kuma wane ne iyalina, da ka kawo ni har zuwa
nan? 17 Kuma sai ka ce wannan bai isa ba a idonka, ya Allah, ka yi magana game
da nan gaba na gidan bawanka. Ka dube ni sai ka ce ni ne mafi ɗaukaka cikin
mutane, ya Ubangiji Allah.
18 "Me kuma Dawuda zai ce maka saboda girmamawar da ka yi wa bawanka?
Gama ka san bawanka, 19 Ya Ubangiji. Gama saboda bawanka da kuma bisa ga
nufinka, ka yi wannan babban abu, ka kuma sanar da dukan manyan alkawura.
20 "Babu wani kamar ka, ya Ubangiji, babu kuma Allah sai kai, kamar yadda
muka ji da kunnuwanmu. 21 Wane ne kuma yake kamar mutanenka Isra'ila,
al'umma guda a duniya wadda Allahnta ya fita don yă fanshi mutane wa kansa,
ya kuma yi suna wa kansa, ya kuma aikata manyan abubuwa masu banmamaki
masu banrazana ta wurin korin al'ummai daga gaban mutanenka, waɗanda ka
fansa daga Masar? 22 Ka mai da mutanenka Isra'ila na kanka har abada, kuma kai,
ya Ubangiji, ka zama Allahnsu.
23 "Yanzu kuwa, Ubangiji, bari alkawarin da ka yi game da bawanka da gidansa
yă kahu har abada. Yi kamar yadda ka yi alkawari, 24 saboda zai kahu kuma
sunanka zai zama mai girma har abada. Sa'an nan mutane za su ce, 'Ubangiji
Maɗaukaki, Allah a bisa Isra'ila, Allahn Isra'ila ne!' Kuma gidan bawanka Dawuda
zai kahu a gabanka.
25 "Kai, Allahna, ka bayyana ga bawanka cewa za ka gina gida dominsa. Ta
haka bawanka ya sami ƙarfin gwiwa ya yi addu'a gare ka. 26 Ya Ubangiji, kai ne
Allah! Ka yi alkawari abubuwa masu kyau wa bawanka. 27 Yanzu ka ji daɗi don
ka albarkace gidan bawanka, don yă ci gaba har abada a gabanka; gama kai, ya
Ubangiji, ka albarkace shi, ya kuma sami albarka ke nan har abada."

# 18

### *Nasarorin Dawuda*
### *(2 Sama'ila 8.1-14)*

1 Ana nan sai Dawuda ya ci Filistiyawa ya kuma rinjaye su, ya ƙwace Gat da
ƙauyukan kewayenta daga mulkin Filistiyawa.
2 Dawuda ya kuma ci Mowabawa, suka zama bayinsa suka kuma biya haraji.
3 Ban da haka, Dawuda ya yaƙi Hadadezer sarkin Zoba, har can Hamat, sa'ad
da ya je don yă kafa mulkinsa a wajen Kogin Yuferites. 4 Dawuda ya kame keken

yaƙinsa dubu ɗaya, da mahayan kekunan yaƙi dubu bakwai da sojojin kafa guda
dubu ashirin. Ya yayyanke dukan agaran dawakansa, amma ya bar dawakai da suka
isa jan kekunan yaƙi ɗari.
5 Da Arameyawan Damaskus suka zo su taimaki Hadadezer sarkin Zoba, sai
Dawuda ya bugi dubu ashirin da biyunsu. 6 Ya sa ƙungiyoyin sojoji a masarautar
Arameyawan Damaskus. Arameyawan kuwa suka zama bayinsa, suka kuma kawo
haraji. Ubangiji ya ba Dawuda nasara a ko'ina da ya tafi.
7 Dawuda ya kwashe garkuwoyin zinariyan da shugabannin sojojin Hadadezer suke
riƙe, ya kawo su Urushalima. 8 Daga Teba da Kun, garuruwan da suke ƙarƙashin
Hadadezer, Dawuda ya kwashe tagulla da yawa sosai, wanda Solomon ya yi amfani
don yă yi Tekun tagulla, ginshiƙai da kuma kayayyakin tagulla dabam-dabam.
9 Sa'ad da Towu sarkin Hamat ya ji cewa Dawuda ya ci mayaƙan Hadadezer sarkin
Zoba gaba ɗaya, 10 sai ya aiki ɗansa Hadoram zuwa wurin Sarki Dawuda yă gaishe
shi yă kuma yi masa barka da nasara a yaƙi a kan Hadadezer, wanda yake yaƙi da
Towu. Hadoram ya kawo kowane irin kayayyakin zinariya da na azurfa da na tagulla.
11 Sarki Dawuda ya miƙa waɗannan kayayyakin ga Ubangiji, kamar yadda ya yi da
azurfa da kuma zinariyan da ya kwaso daga dukan waɗannan al'ummai. Edom da
Mowab, Ammonawa da Filistiyawa, da kuma Amalek.
12 Abishai ɗan Zeruhiya ya bugi mutanen Edom dubu goma sha takwas a Kwarin
Gishiri. 13 Ya sa ƙungiyoyin sojoji a Edom, dukan mutanen Edom kuwa suka zama
bayin Dawuda. Ubangiji ya ba Dawuda nasara a ko'ina da ya tafi.

### *Manyan ma'aikatan Dawuda*
### *(2 Sama'ila 8.15-18)*

14 Dawuda ya yi mulki a bisa dukan Isra'ila, yana yin abin da yake daidai da kuma
gaskiya saboda dukan mutanensa.

15 Yowab ɗan Zeruhiya shi ne shugaban mayaƙa;
Yehoshafat ɗan Ahilud shi ne marubuci;
16 Zadok ɗan Ahitub da Abimelek ɗan Abiyatar su ne firistoci;
Shafsha shi ne magatakarda;
17 Benahiya ɗan Yehohiyada shi ne shugaban Keretawa da Feletiyawa;
'ya'yan Dawuda maza su ne manyan ma'aikata a gefen sarki.

# 19

### *Dawuda ya ci Ammonawa da yaƙi*
### *(2 Sama'ila 10.1-19)*

1 Ana nan, sai Nahash sarkin Ammonawa ya mutu, sai ɗansa ya gāje shi a matsayin
sarki. 2 Dawuda ya yi tunani, "Zan nuna jinƙai ga Hanun ɗan Nahash, domin
mahaifinsa ya nuna alheri gare ni." Saboda haka Dawuda ya aika da tawaga don
yă yi wa Hanun ta'aziyya game da mahaifinsa.
Sa'ad da mutanen Dawuda suka iso wurin Hanun a ƙasar Ammonawa don su
ta'azantar da shi, 3 sai manyan Ammonawa suka ce wa Hanun, "Kana tsammani
Dawuda yana girmama mahaifinka ne da ya aika mutanen nan wurinka su ta'azantar
da kai? Ba mutanensa sun zo ne su bincika su kuma leƙi ƙasar su tumɓuke ta ba?"
4 Saboda haka Hanun ya kama mutanen Dawuda, ya yi musu aski, ya yayyanka
rigunansu a daidai ɗuwawunsu, sa'an nan ya sallame su.
5 Da wani ya zo ya faɗa wa Dawuda game da mutanen, sai ya aiki 'yan aika su
sadu da su, gama an ƙasƙantar da su ainun. Sarki ya ce, "Ku zauna a Yeriko har sai
gemunku sun yi girma, sa'an nan ku dawo."

6 Sa’ad da Ammonawa suka gane cewa sun zama abin wurin a kafan hancin
Dawuda, Hanun da Ammonawa suka aika da talenti dubu na azurfa don su yi haya
da kekunan yaƙi da mahayan kekunan yaƙi daga Aram-Naharayim, Aram Ma’aka da
Zoba. 7 Suka yi hayar kekunan yaƙi da mahayan kekunan yaƙi dubu talatin da biyu,
da kuma sarkin Ma’aka tare da mayaƙansa, waɗanda suka zo suka kafa sansani kusa
da Medeba, yayinda Ammonawa suka tattaru daga garuruwansu suka fita yaƙi.
8 Da jin haka, Dawuda ya aiki Yowab tare da dukan mayaƙa masu yaƙi.
9 Ammonawa suka fito suka ja dāgā a ƙofar birninsu, yayinda sarakunan da suka
zo, su kansu suka ware suna a fili.
10 Yowab ya ga cewa akwai dāgā a gabansa da bayansa; sai ya zaɓi waɗansu
mayaƙa mafi kyau a Isra’ila ya sa su a kan Arameyawa. 11 Ya sa sauran mutanen
a ƙarƙashin kulawar Abishai ɗan’uwansa, aka sa a kan Ammonawa. 12 Yowab ya ce,
“In Arameyawa suka fi ni ƙarfi, sai ka kawo mini ɗauke da ni; amma in Ammonawa
sun fi ka ƙarfi, sai in kawo maka ɗauke. 13 Ka yi ƙarfin hali bari mu yi yaƙi da
jaruntaka saboda mutanenmu da biranen Allahnmu. UBANGIJI zai yi abin da ya ga ya
yi masa kyau.”
14 Sai Yowab da ƙungiyoyin mayaƙan da suke tare da shi suka matso don su yi yaƙi
da Arameyawa, Arameyawan kuwa suka gudu a gabansa. 15 Sa’ad da Ammonawa
suka ga Arameyawa suna gudu, sai su ma suka guda a gaban ɗan’uwansa Abishai
suka shiga cikin birni. Sai Yowab ya koma Urushalima.
16 Bayan Arameyawa suka ga cewa Isra’ila sun ci su da yaƙi, sai suka aiki ’yan
aika suka sa aka kawo Arameyawan da suke hayen Kogi waɗanda Shobak shugaban
mayaƙan Hadadezer yake shugabanta.
17 Sa’ad da aka faɗa wa Dawuda wannan, sai tattara dukan Isra’ila ya haye Urdun;
ya tafi wurinsu ya kuwa ja dāgā ɗaura da su. Dawuda ya ja dāgārsa don yă sadu da
Arameyawa a yaƙi, su kuwa suka yi yaƙi da shi. 18 Amma Arameyawa suka gudu a
gaban Isra’ila, mutanen Dawuda kuwa suka kashe masu hawan keken yaƙinsu dubu
bakwai da sojojin ƙasa dubu arba’in. Ya kuma kashe Shobak shugaban mayaƙansu.
19 Da abokan tarayyar Hadadezer suka ga Isra’ila sun ci su da yaƙi, sai suka nemi
salama da Dawuda suka kuma zama bayinsa.
Saboda haka Arameyawa ba su ƙara yarda su taimaki Ammonawa ba.

# 20

*An ci Rabba*
*(2 Sama’ila 11.1; 12.26-31)*

1 Da bazara, a lokacin da sarakuna kan tafi yaƙi, Yowab ya jagorance mayaƙa. Ya
lalatar da ƙasar Ammonawa ya kuma tafi Rabba ya yi mata kwanto, amma Dawuda
ya zauna a Urushalima. Yowab ya yaƙi Rabba, ya kuma bar ta kango. 2 Dawuda ya
ɗauki rawani daga kan sarkinsu, nauyinsa ya kai talenti na zinariya, aka kuma yi
masa ado da duwatsu masu daraja, sai Dawuda kuwa ya sa a kansa. Ya kuma kwashi
ganima mai yawa daga birnin 3 ya kuma fitar da mutanen da suke can, ya sa su aiki
da zartuna da makamai masu kaifi da kuma gatura. Dawuda ya yi haka da dukan
garuruwan Ammonawa. Sa’an nan Dawuda da mayaƙansa gaba ɗaya suka koma
Urushalima.

*Yaƙi da Filistiyawa*
*(2 Sama’ila 21.15-22)*

4 Ana nan, sai yaƙi ya ɓarke a Gezer tsakanin Isra’ila da Filistiyawa. Sai Sibbekai
mutumin Husha ya kashe Siffai, ɗaya daga cikin zuriyar Refahiyawa, ta haka kuma
aka ci Filistiyawa da yaƙi.

5 Yaƙi kuma ya sāke tashi tsakanin Isra'ilawa da Filistiyawa, Elhanan ɗan Yayir ya
kashe Lahmi ɗan'uwan Goliyat mutumin Gat, wanda yake riƙe da māshi mai sandan
masaƙa.
6 Aka sāke yin wani yaƙin kuma, wanda ya faru a Gat, akwai wani ƙaton mutum
mai yatsotsi shida a kowane hannu da kuma yatsotsi shida a kowace ƙafa, yatsotsi
ashirin da huɗu ke nan. Shi ma daga zuriyar Rafa ce. 7 Sa'ad da ya yi wa Isra'ila
ba'a, sai Yonatan ɗan Shimeya, ɗan'uwan Dawuda ya kashe shi.
8 Waɗannan su ne zuriyar Rafa a Gat, Dawuda da mutanensa sun kashe su.

# 21

*Dawuda ya ƙidaya mayaƙansa*
*(2 Sama'ila 24.1-9)*
1 Sai Shaiɗan ya tashi gāba da Isra'ila, ya zuga Dawuda ya ƙidaya Isra'ila. 2 Saboda
haka Dawuda ya ce wa Yowab da shugabannin mayaƙa, "Ku tafi ku ƙidaya Isra'ilawa
daga Beyersheba zuwa Dan. Ku kawo mini labarin saboda in san su nawa ne."
3 Amma Yowab ya amsa ya ce, "Ubangiji ya riɓaɓɓanya mayaƙansa fiye da sau
ɗari. Ranka yă daɗe sarki, dukansu ba bayin shugabana ba ne? Me ya sa ranka yă
daɗe yake so yă yi haka? Me zai sa ka kawo laifi a kan Isra'ila?"
4 Amma sarki ya nace a kan maganar da ya yi wa Yowab. Sai Yowab ya tashi
ya tafi cikin dukan Isra'ila, ya kewaye sa'an nan ya dawo Urushalima. 5 Yowab ya
ba labarin yawan mayaƙan wa Dawuda. A cikin Isra'ila akwai mutum miliyon da
dubu ɗari ɗaya waɗanda za su iya riƙe takobi, haɗe da dubu ɗari huɗu da saba'in
a Yahuda.
6 Amma Yowab bai haɗa da mutanen Lawi da na Benyamin a ƙidayar ba, domin
bai ji daɗin umarnin sarki ba.
*(2 Sama'ila 24.10-17)*
7 Wannan umarnin mugu ne a gaban Allah; saboda haka ya hukunta Isra'ila.
8 Sai Dawuda ya ce wa Allah, "Na yi zunubi ƙwarai ta wurin yin wannan. Yanzu,
na roƙe ka, ka ɗauke laifin bawanka. Na yi wauta sosai."
9 Sai Ubangiji ya ce wa Gad, mai duba na Dawuda, 10 "Tafi ka faɗa wa Dawuda,
'Ga abin da Ubangiji ya ce ina ba ka abubuwa uku. Ka zaɓi ɗaya daga cikinsu don
in aikata a kanka.' "
11 Saboda haka Gad ya tafi wurin Dawuda ya ce masa, "Ga abin da Ubangiji ya
ce, 'Ka yi zaɓi, 12 shekara uku na yunwa, wata uku na shan ɗibga a gaban abokan
gābanka, sa'ad da za su bi suna kakkashe ku, ko kuwa kwana uku na takobin
Ubangiji, ranakun annoba a cikin ƙasar, mala'ikan Ubangiji zai hallaka kowane sashe
na Isra'ila.' Yanzu sai ka yanke shawara yadda zan amsa wa wanda ya aiko ni."
13 Dawuda ya ce wa Gad, "Na shiga uku. Bari in fāɗa a hannuwan Ubangiji, gama
jinƙansa yana da girma sosai; amma kada ka bari in fāɗa a hannuwan mutane."
14 Sai Ubangiji ya aiko da annoba a kan Isra'ila, mutane duba saba'in na Isra'ila
suka mutu. 15 Allah kuwa ya aiki mala'ika yă hallaka Urushalima. Amma yayinda
mala'ikan yana gab da yin haka, sai Ubangiji ya gani ya kuma yi nadama saboda
masifar, sai ya ce wa mala'ikan wanda yake hallaka mutane, "Ya isa! Janye
hannunka." Mala'ikan Ubangiji kuwa yana tsaye a masussukar Ornan mutumin
Yebus.
16 Sai Dawuda ya ɗaga ido ya ga mala'ikan Ubangiji tsaye tsakanin sama da duniya,
da takobi a zāre a hannunsa ya miƙa a kan Urushalima. Sai Dawuda da dattawa, saye
da rigunan makoki suka fāɗi rubda jiki.
17 Dawuda ya ce wa Allah, "Ba ni ba ne na umarta a ƙidaya mayaƙan? Ni ne wanda
ya yi zunubin da kuma abin da ba daidai ba. Waɗannan dai tumaki ne. Me suka yi?

Ya Ubangiji Allahna, bari hannunka ya fāɗi a kaina da kuma iyalina, amma kada ka
bar wannan annoba ya kasance a kan mutanenka.”

*(2 Sama’ila 24.18-25)*

18 Sa’an nan mala’ikan Ubangiji ya umarci Gad yă faɗa wa Dawuda yă haura
yă gina bagade wa Ubangiji a masussukar Ornan mutumin Yebus. 19 Saboda haka
Dawuda ya haura cikin biyayya ga maganar da Allah ya yi da sunan Ubangiji.
20 Yayinda Ornan yake sussukar alkama, sai ya juya ya ga mala’ika; ’ya’yansa maza
guda huɗu da suke tare da shi suka ɓuya. 21 Sai Dawuda ya kusato, sa’ad da Ornan
ya duba sai ya gan shi, ya bar masussukar ya rusuna a gaban Dawuda da fuskarsa
har ƙasa.
22 Dawuda ya ce wa Ornan, “Ka ba ni masussukarka saboda in gina bagade wa
Ubangiji, don annobar da take kan mutane tă daina. Ka sayar mini ita a cikakken
kuɗinta.”
23 Ornan ya ce wa Dawuda, “Ka karɓa! Bari ranka yă daɗe, sarki yă yi duk abin da
ya ga ya yi masa kyau. Duba, zan ba da shanu domin hadaya ta ƙonawa, da itacen
sussuka, da kuma alkama domin hadaya ta gari. Zan ba da dukan wannan.”
24 Amma Sarki Dawuda ya amsa wa Ornan ya ce, “A’a, na nace zan biya cikakken
kuɗinta. Ba zan karɓi abinka kawai don Ubangiji ba, ko in miƙa hadaya ta ƙonawar
da ba tă ci mini wani abu ba.”
25 Saboda haka Dawuda ya biya Ornan shekel ɗari shida na zinariya saboda wurin.
26 Dawuda ya gina bagade wa Ubangiji a can ya kuma miƙa hadayu na ƙonawa da
hadayu na salama, Ubangiji kuwa ya amsa masa ta wurin wuta daga sama a kan
bagaden hadaya ta ƙonawa.
27 Sa’an nan Ubangiji ya yi magana ga mala’ikan, ya kuma mayar da takobinsa a
kube. 28 A lokacin, sa’ad da Dawuda ya ga cewa Ubangiji ya amsa masa a masussukar
Ornan mutumin Yebus, sai ya miƙa hadayu a can. 29 Tabanakul na Ubangiji da Musa
ya yi a hamada, da kuma bagaden hadaya ta ƙonawa a lokacin suna a tudun Gibeyon.
30 Amma Dawuda bai iya zuwa gabansa don yă yi tambaya ga Allah ba, gama yana
jin tsoron takobin mala’ikan Ubangiji.

## 22

1 Sai Dawuda ya ce, “Gidan Ubangiji Allah zai kasance a nan, haka kuma bagaden
hadaya ta ƙonawa don Isra’ila.”

*Shirye-shirye don haikali*

2 Dawuda kuwa ya umarta a tattara baƙin da suke zama a Isra’ila, daga cikinsu ya
sa masu farfasa duwatsu don su shirya duwatsun da aka sassaƙa saboda ginin gidan
Allah. 3 Ya tanada ƙarfe mai yawa don ƙusoshi saboda ƙyamaren hanyoyin shiga da
kuma saboda mahaɗai, da ƙarin tagulla fiye da ƙirge. 4 Ya kuma tanada gumaguman
al’ul masu yawa fiye da ƙirge, gama Sidoniyawa da mutanen Taya sun kawo su wa
Dawuda da yawa.
5 Dawuda ya ce, “Dana Solomon matashi ne kuma bai gogu ba, kuma gidan da za
a gina wa Ubangiji zai zama mai ƙayatarwa ƙwarai, sananne da kuma mai daraja a
idon dukan al’ummai. Saboda haka zan yi shirye-shirye saboda shi.” Sai Dawuda ya
yi ɗumbun shirye-shirye kafin mutuwarsa.
6 Sa’an nan ya kira ɗansa Solomon ya umarce shi yă gina gida domin Ubangiji,
Allah na Isra’ila. 7 Dawuda ya ce wa Solomon, “Dana, na yi niyya a zuciyata in gina
gida saboda Sunan Ubangiji Allahna. 8 Amma wannan maganar Ubangiji ta zo mini,
‘Ka zub da jini mai yawa ka kuma yi yaƙe-yaƙe masu yawa. Ba za ka gina gida
domin Sunana ba, domin ka zub da jini da yawa a duniya a idona. 9 Amma za ka
haifi ɗa wanda zai zama mutumin salama da kuma hutu, zan kuma ba shi hutu daga

dukan abokan gābansa a kowane gefe. Za a kira shi Solomon, zai kuma kawo wa
Isra'ila salama da natsuwa a zamanin mulkinsa. 10 Shi ne wanda zai gina gida saboda
Sunana. Zai zama ɗana, ni kuma zan zama mahaifinsa. Zan kafa kujerar sarautarsa
a bisa Isra'ila har abada.'
11 "Yanzu, ɗana, UBANGIJI ya kasance tare da kai, bari kuma ka yi nasara ka kuma
gina gidan UBANGIJI Allahnka, kamar yadda ya ce za ka yi. 12 Bari UBANGIJI ya ba ka
basira da fahimi sa'ad da ya sa ka shugaba a bisa Isra'ila, saboda ka kiyaye dokar
UBANGIJI Allahnka. 13 Ta haka za ka yi nasara in ka mai da hankali ga kiyaye ƙa'idodi
da dokokin da UBANGIJI ya ba wa Musa saboda Isra'ila. Ka yi ƙarfin hali ka kuma
ƙarfafa. Kada ka ji tsoro ko ka fid da zuciya.
14 "Na sha wahala da yawa don in yi tanadi talentin dubu ɗari na zinariya, talenti
miliyon na azurfa, ɗumbun tagulla da ƙarfe da suka wuce ƙirge da katako da dutse
saboda haikalin UBANGIJI. Za ka iya ƙara su. 15 Kana da ma'aikata masu yawa, masu
fafarshe duwatsu, masu gini da masu aikin katako, da kuma gwanaye a kowane irin
aikin 16 zinariya da azurfa, tagulla da ƙarfe, masu sana'a waɗanda suka wuce ƙirge.
Yanzu ka fara aiki, UBANGIJI kuma ya kasance tare da kai."
17 Sai Dawuda ya umarta dukan shugabannin Isra'ila su taimake ɗansa Solomon.
18 Ya ce musu, "Ba UBANGIJI Allahnku yana tare da ku ba? Bai kuma ba ku hutu a
kowane gefe ba? Gama ya ba da mazaunan ƙasar gare ni, ƙasar kuma ta UBANGIJI ce
da mutanensa. 19 Yanzu fa sai ku sa zuciyarku da ranku ga neman UBANGIJI Allahnku.
Ku fara ginin wuri mai tsarki na UBANGIJI Allah, don ku kawo akwatin alkawarin
UBANGIJI da kayayyaki masu tsarki na Allah a cikin haikalin da za a gina saboda
Sunan UBANGIJI."

# 23

*Lawiyawa*

1 Sa'ad da Dawuda ya tsufa yana kuma da cikakken shekaru, ya sa ɗansa Solomon
sarki bisa Isra'ila.
2 Ya kuma tattara dukan shugabannin Isra'ila a wuri ɗaya, haka kuma ya yi da
firistoci da Lawiyawa. 3 Aka ƙidaya Lawiyawan da suke 'yan shekaru talatin da
haihuwa ko fiye, suka kai wajen mutum dubu talatin da takwas. 4 Dawuda ya ce,
"Cikin waɗannan, dubu ashirin da huɗu za su lura da aikin haikalin UBANGIJI, dubu
shida su zama manyan na ma'aikata da alƙalai. 5 Dubu huɗu su zama matsaran
ƙofofi, dubu huɗu kuma su yabi UBANGIJI da kayayyakin bushe-bushe da na kaɗe-
kaɗe waɗanda na tanada saboda wannan manufa."

6 Dawuda ya rarraba Lawiyawa ƙungiya-ƙungiya bisa ga 'ya'yan Lawi maza.
Gershon, Kohat da Merari.

*Gershon*

7 Na Gershonawa,
Ladan da Shimeyi.
8 'Ya'yan Ladan maza su ne,
Yehiyel na farko, Zetam da Yowel, su uku ne duka.
9 'Ya'yan Shimeyi maza su ne,
Shelomot, Haziyel da Haran, su uku ne duka.
Waɗannan su ne kawunan iyalan Ladan.
10 'Ya'yan Shimeyi maza kuwa su ne,
Yahat, Zina, Yewush da Beriya.
Waɗannan su ne 'ya'yan Shimeyi maza, su huɗu ne duka.

11 Yahat shi ne na fari, Ziza kuma na biyu, amma Yewush da Beriya ba su haifi
'ya'ya maza da yawa ba; saboda haka aka ƙidaya su kamar iyali ɗaya a wurin rabon aiki.

*Kohatawa*

12 'Ya'yan Kohat maza su ne,
Amram, Izhar, Hebron da Uzziyel, su huɗu ne duka.
13 'Ya'yan Amram maza su ne,
Haruna da Musa.
Haruna shi ne aka keɓe, shi da zuriyarsa har abada, don su tsarkake kayayyakin
mafi tsarki, su miƙa hadayu a gaban UBANGIJI, su yi hidima a gabansa su kuma
furta albarku a cikin sunansa har abada. 14 An ƙidaya aka kuma haɗa 'ya'yan
Musa maza mutumin Allah a sashen kabilar Lawi.
15 'Ya'yan Musa maza su ne,
Gershom da Eliyezer.
16 Zuriyar Gershom su ne,
Shebuwel ne ɗan fari.
17 Zuriyar Eliyezer su ne,
Rehabiya ne ɗan fari.
Eliyezer ba shi da waɗansu 'ya'ya maza, amma 'ya'yan Rehabiya maza sun yi yawa.
18 'Ya'yan Izhar maza su ne,
Shelomit ne ɗan fari.
19 'Ya'yan Hebron maza su ne,
Yeriya na fari, Amariya na biyu, Yahaziyel na uku da Yekameyam na huɗu.
20 'Ya'yan Uzziyel maza su ne,
Mika na fari da Isshiya na biyu.

*Merariyawa*

21 'Ya'yan Merari maza su ne,
Mali da Mushi.
'Ya'yan Mali maza su ne,
Eleyazar da Kish.
22 Eleyazar ya mutu ba 'ya'yan maza, yana da 'ya'ya mata ne kawai.
'Yan'uwansu, 'ya'yan Kish maza, suka aure su.
23 'Ya'yan Mushi maza su ne,
Mali, Eder da Yeremot, su uku ne duka.

24 Waɗannan ne zuriyar Lawi bisa ga iyalansu, kawunan iyalai kamar yadda
aka rubuta su a ƙarƙashin sunayensu aka kuma ƙirga kowa, wato, masu
aikin da suke 'yan shekara ashirin da haihuwa ko fiye waɗanda suka yi
hidima a cikin haikalin UBANGIJI. 25 Gama Dawuda ya ce, "Tun da UBANGIJI,
Allah na Isra'ila, ya ba da hutu ga mutanensa, ya kuma zo ya zauna a
Urushalima har abada, 26 Lawiyawa ba sa ƙara bukata su ɗauki tabanakul
ko kuwa waɗansu kayayyakin da ake amfani da su a hidima." 27 Bisa ga
umarnin ƙarshe na Dawuda, za a ƙidaya Lawiyawa daga 'yan shekara
ashirin ko fiye.

28 Aikin Lawiyawa shi ne su taimaki zuriyar Haruna a hidimar haikalin UBANGIJI;
su lura da filaye da kuma ɗakunan da suke gefe, su tsarkake dukan kayayyaki masu
tsarki, su kuma yi waɗansu ayyuka a gidan Allah. 29 Su ne za su lura da burodin
da aka ajiye a tebur, lallausan gari don hadaya ta gari, waina marar yisti, toyawa da

kwaɓawa, da kuma dukan awon yawa da kuma girman abubuwa. 30 Su ne kuma za
su tsaya kowace safiya su yi godiya, su kuma yabi UBANGIJI. Za su kuma yi haka da
yamma 31 da kuma a duk sa'ad da aka miƙa hadayun ƙonawa ga UBANGIJI a Asabbatai
da bukukkuwan Sabon Wata da kuma a ƙayyadaddun bukukkuwa, za su yi hidima
a gaban UBANGIJI kullum bisa ga yawan da aka tsara da kuma a hanyar da aka tsara
musu.
32 A haka kuwa Lawiyawa suka yi ayyukansu don Tentin Sujada, don Wuri Mai
Tsarki da kuma a ƙarƙashin 'yan'uwansu zuriyar Haruna, saboda hidimar haikalin
UBANGIJI.

# 24

*Sassan firistoci*

1 Waɗannan su ne sassan 'ya'yan Haruna maza.

'Ya'yan Haruna maza su ne Nadab, Abihu, Eleyazar da Itamar. 2 Amma Nadab
da Abihu sun mutu kafin mahaifinsu, ba su kuma haifi 'ya'ya maza ba; saboda
haka Eleyazar da Itamar suka yi hidimar firistoci. 3 Tare da taimakon Zadok zuriyar
Eleyazar da Ahimelek wani zuriyar Itamar. Dawuda ya karkasa su zuwa ɓangarori
don aikinsu bisa ga hidima. 4 Akwai ɗumbun shugabanni a cikin zuriyar Eleyazar
fiye da zuriyar Itamar, aka kuma karkasa su haka, kawuna goma sha shida daga
zuriyar Eleyazar da kuma kawuna iyalai takwas daga zuriyar Itamar. 5 Aka karkasa
su babu sonkai ta wurin jifa ƙuri'a, gama akwai manyan ma'aikatan wuri mai tsarki
da manyan ma'aikatan Allah a cikin zuriyar Eleyazar da Itamar.

6 Shemahiya ɗan Netanel, wani Balawe ne marubuci, ya rubuta sunayensu a gaban
sarki da kuma a gaban manyan ma'aikata. Zadok firist, Ahimelek ɗan Abiyatar da
kuma kawunan iyalan firistoci da na Lawiyawa, iyali guda daga Eleyazar, guda kuma
daga Itamar.

7 Kuri'a ta farko ta faɗa a kan Yehoyarib,
na biyu a kan Yedahiya,
8 na uku a kan Harim,
na huɗu a kan Seyorim,
9 na biyar a kan Malkiya,
na shida a kan Miyamin,
10 na bakwai a kan Hakkoz,
na takwas a kan Abiya,
11 na tara a kan Yeshuwa,
na goma a kan Shekaniya,
12 na goma sha ɗaya a kan Eliyashib,
na goma sha biyu a kan Yakim,
13 na goma sha uku a kan Huffa,
na goma sha huɗu a kan Yeshebeyab,
14 na goma sha biyar a kan Bilga,
na goma sha shida a kan Immer,
15 na goma sha shida a kan Hezir,
na goma sha takwas a kan Haffizzez,
16 na goma sha tara a kan Fetahahiya,
na ashirin a kan Ezekiyel,
17 na ashirin da ɗaya wa Yakin,
na ashirin da biyu a kan Gamul,
18 na ashirin da uku wa Delahiya

da kuma na ashirin da huɗu a kan Ma'aziya.

19 Ga tsarin aikinsu na hidima sa'ad da suka shiga haikalin UBANGIJI, bisa ga ƙa'idar
da kakansu Haruna ya kafa, yadda UBANGIJI, Allah na Isra'ila ya umarce shi.

### *Sauran Lawiyawa*

20 Game da sauran zuriyar Lawi kuwa,

Daga 'ya'yan Amram maza. Shubayel;
daga 'ya'yan Shubayel maza. Yedehiya.
21 Game da Rehabiya kuwa, daga 'ya'yansa maza. Isshiya shi ne na fari.
22 Daga mutanen Izhar, Shelomot;
daga 'ya'yan Shelomot maza, Yahat.
23 'Ya'yan Hebron maza su ne, Yeriya na fari, Amariya na biyu, Yahaziyel na uku
da Yekameyam na huɗu.
24 Ɗan Uzziyel shi ne, Mika;
daga 'ya'yan Mika maza, Shamir.
25 Ɗan'uwan Mika shi ne, Isshiya;
daga 'ya'yan Isshiya maza, Zakariya.
26 'Ya'yan Merari su ne, Mali da Mushi.
Ɗan Ya'aziya shi ne, Beno.
27 'Ya'yan Merari su ne,
daga Ya'aziya, Beno, Shoham, Zakkur da Ibri.
28 Daga Mali, Eleyazar, wanda ba shi da 'ya'ya maza.
29 Daga Kish, ɗan Kish shi ne,
Yerameyel.
30 Kuma 'ya'yan Mushi maza su ne, Mali, Eder da Yerimot.

Waɗannan su ne Lawiyawa bisa ga iyalansu.

31 Suka kuma jifa ƙuri'a, kamar dai yadda 'yan'uwansu zuriyar Haruna suka yi, a
gaban Sarki Dawuda da gaban Zadok, Ahimelek, da kuma a gaban kawunan iyalan
firistoci da na Lawiyawa. Aka yi da iyalan wa daidai da iyalan ƙane.

## 25

### *Mawaƙa*

1 Dawuda tare da shugabannin mayaƙa, suka keɓe waɗansu daga 'ya'yan Asaf,
Heman da Yedutun don hidimar yin annabci, suna amfani da garayu, molaye da
ganguna. Ga jerin mutanen da suka yi wannan hidima.

2 Daga 'ya'yan Asaf,
Zakkur, Yusuf, Netaniya da Asarela. 'Ya'yan Asaf sun kasance a ƙarƙashin
kulawar Asaf, wanda ya yi annabci a ƙarƙashin kulawar sarki.
3 Game da Yedutun kuwa, daga 'ya'yansa maza.
Gedaliya, Zeri, Yeshahiya, Shimeyi, Hashabiya da Mattitiya, su shida ne duka, a
ƙarƙashin kulawar mahaifinsu Yedutun, wanda ya yi annabci, yana amfani da
garaya a yin godiya da yabon UBANGIJI.
4 Game da Heman kuwa, daga 'ya'yansa maza.
Bukkiya, Mattaniya, Uzziyel, Shebuwel, Yerimot; Hananiya, Hanani, Eliyata,
Giddalti, Romamti-Ezer, Yoshbekasha, Malloti, Hotir da Mahaziyot. 5 Dukan
waɗannan 'ya'yan Heman ne mai duba na sarki. An ba shi su ta wurin

alkawarin Allah don yă ɗaukaka shi. Allah ya ba Heman ʼyaʼya maza goma sha huɗu da ʼyaʼya mata uku.

6 Dukan waɗannan mutane suna a ƙarƙashin kulawar mahaifansu don kaɗe-kaɗe
da bushe-bushe a cikin haikalin UBANGIJI, da ganguna, molaye da garayu, don hidima
a gidan Allah.

Asaf, Yedutun da Heman suna ƙarƙashin kulawar sarki. 7 Da su da danginsu,
dukansu su 288 ne kuma horarru da ƙwararru ne a kaɗe-kaɗe da bushe-bushe domin
UBANGIJI. 8 Baba ko yaro, malami ko ɗalibi, duk suka jefa ƙuriʼa saboda ayyukan da
za su yi.

9 Kuriʼa ta fari, wadda take don Asaf, ta fāɗo a kan Yusuf, ʼyaʼyansa maza da danginsa, 12

ta biyu a kan Gedaliya, danginsa da ʼyaʼyansa maza, 12

10 ta uku a kan Zakkur, ʼyaʼyansa da danginsa, 12

11 ta huɗu a kan Izri, ʼyaʼyansa maza da danginsa, 12

12 ta biyar a kan Netaniya, ʼyaʼyansa maza da danginsa, 12

13 ta shida a kan Bukkiya, ʼyaʼyansa maza da danginsa, 12

14 ta bakwai a kan Yesarela, ʼyaʼyansa maza da danginsa, 12

15 ta takwas a kan Yeshahiya, ʼyaʼyansa maza da danginsa, 12

16 ta tara a kan Mattaniya, ʼyaʼyansa maza da danginsa, 12

17 ta goma a kan Shimeyi, ʼyaʼyansa maza da danginsa, 12

18 ta goma sha ɗaya a kan Azarel, ʼyaʼyansa maza da danginsa, 12

19 ta goma sha biyu a kan Hashabiya, ʼyaʼyansa maza da danginsa, 12

20 ta goma sha uku a kan Shubayel, ʼyaʼyansa maza da danginsa, 12

21 ta goma sha huɗu a kan Mattitiya, ʼyaʼyansa maza da danginsa, 12

22 ta goma sha biya a kan Yeremot, ʼyaʼyansa maza da danginsa, 12

23 ta goma sha shida a kan Hananiya, na goma sha biya a kan Yerimot, ʼyaʼyansa maza da danginsa, 12

24 ta goma sha bakwai a kan Yoshbekasha, na goma sha biya a kan Yerimot, ʼyaʼyansa maza da danginsa, 12

25 ta goma sha takwas a kan Hanani, na goma sha biya a kan Yerimot, ʼyaʼyansa maza da danginsa 12

26 ta goma sha tara a kan Malloti, na goma sha biya a kan Yerimot, ʼyaʼyansa maza da danginsa, 12

27 ta ashirin a kan Eliyata, na goma sha biya a kan Yerimot, ʼyaʼyansa maza da danginsa, 12

28 ta ashirin da ɗaya a kan Hotir, na goma sha biya a kan Yerimot, ʼyaʼyansa maza da danginsa, 12

29 ta ashirin da biyu a kan Giddalti, na goma sha biya a kan Yerimot, ʼyaʼyansa maza da danginsa, 12

30 ta ashirin da uku a kan Mahaziyot, na goma sha biya a kan Yerimot, ʼyaʼyansa maza da danginsa, 12

31 ta ashirin da huɗu a kan Romamti-Ezer, na goma sha biya a kan Yerimot, ʼyaʼyansa maza da danginsa 12.

# 26

*Matsaran ƙofofi*

1 Ɓangarorin Matsaran Kofofi su ne,

Daga Korayawa,
Meshelemiya ɗan Kore, ɗaya daga cikin ʼyaʼyan Asaf maza. 2 Meshelemiya yana
da ʼyaʼya maza.
Zakariya ɗan fari, Yediyayel na biyu,
Zebadiya na uku, Yatniyel na huɗu,
3 Elam na biyar, Yehohanan na shida
da Eliyehoyenai na bakwai.
4 Obed-Edom shi ma yana da ʼyaʼya maza.
Shemahiya ɗan fari, Yehozabad na biyu,
Yowa na uku, Sakar na huɗu
Netanel na biyar, 5 Ammiyel na shida,
Issakar na bakwai da Feyuletai na takwas.
(Gama Allah ya albarkace Obed-Edom.)
6 Ɗan Obed-Edom, wato, Shemahiya shi ma yana da ʼyaʼya maza, waɗanda suke
shugabanni a cikin iyalin mahaifinsu, gama su jarumawa ne ƙwarai. 7 ʼYaʼyan
Shemahiya maza su ne,
Otni, Rafayel, Obed da Elzabad;
danginsa Elihu da Shemahiya su ma jarumawa ne.
8 Ɗaukan waɗannan zuriyar Obed-Edom ne; su da ʼyaʼyansu maza da
danginsu, jarumawa ne masu ƙarfin yin aiki. Zuriyar Obed-Edom, mutum
62 ne duka.
9 Meshelemiya yana da ʼyaʼya maza da kuma ʼyanʼuwa, waɗanda jarumawa
ne, su 18 ne duka.

10 Hosa dangin Merari yana da ʼyaʼya maza.
Shimri na fari (ko da yake ba shi ne ɗan fari ba, mahaifinsa ya sa shi na fari),
11 Hilkiya ne na biyu, Tabaliya ne na uku
sai kuma Zakariya na huɗu.
ʼYaʼya da dangin Hosa su 13 ne duka.

12 Waɗannan ɓangarori na matsaran ƙofofi, ta wurin manyansu, suna da
ayyukan yin hidima a haikalin Ubangiji, kamar yadda danginsu suke da
shi. 13 Aka jefa ƙuriʼu don kowace ƙofa bisa ga iyalansu, ƙarami da babba.
14 Kuriʼa don Kofar Gabas ta fāɗo a kan Shelemiya.
Sai aka jefa ƙuriʼu don ɗansa Zakariya, mai ba da shawara mai maʼana, sai ƙuriʼa
ta ƙofar arewa ta fāɗo a kansa.
15 Kuriʼa don Kofar Kudu ta fāɗo a kan Obed-Edom, ƙuriʼa don ɗakin ajiya kuwa
ta fāɗo a kan ʼyaʼyansa maza.
16 Kuriʼu don Kofar Yamma da kuma Kofar Shalleket a hanyar bisa suka fāɗo a kan
Shuffim da Hosa.

Aikin tsaro bisa ga mai tsaro.
17 Akwai Lawiyawa shida da suke tsaron ƙofar gabas,
huɗu a ƙofar kudu,
huɗu kuma a ƙofar arewa,
biyu-biyu suke tsaron ɗakunan ajiya.
18 Game da filin waje ta yamma kuwa, akwai masu tsaro huɗu a hanya da kuma
biyu a filin* kansa.

* **26:18** Maʼanar wannan a Ibraniyanci babu tabbas.

19 Waɗannan su ne ɓangarori na matsaran ƙofofi waɗanda suke zuriyar Kora
da Merari.

*Masu ajiya da sauran manyan ma'aikata*

20 'Yan'uwansu Lawiyawa kuwa su ne[†] suke lura da ma'ajin gidan Allah da kuma
baitulmali don kayayyakin da aka keɓe.
21 Ladan ɗan Gershon ne, kuma kaka ga iyalai masu yawa, har ma da iyalin ɗansa
Yehiyeli, 22 'ya'yan Yehiyeli maza su ne, Zetam da ɗan'uwansa Yowel. Su ne suke
kula da ma'ajin haikalin UBANGIJI.

23 Daga zuriyar Amram, Izhar, mutanen Hebron da kuma Uzziyel, su ma aka
ba su aiki.

24 Shebuwel ɗan Gershom, daga zuriyar Musa, shi ne babban jami'i mai lura da
baitulmali. 25 Danginsa na wajen Eliyezer su ne, Rehabiya, Yeshahiya, Yoram,
Zikri da Shelomit.
26 Shelomit da danginsa su ne suke lura da dukan baitulmali don kayayyakin da
Sarki Dawuda ya keɓe, ta wajen kawunan iyalai waɗanda suke shugabannin
dubu-dubu da shugabannin ɗari-ɗari, da kuma wajen sauran shugabannin
mayaƙa. 27 Sun keɓe waɗansu ganimar da aka kwaso a yaƙi don gyaran
haikalin UBANGIJI. 28 Shelomit da 'yan'uwansa suka lura da dukan abubuwan
da annabi Sama'ila da Shawulu ɗan Kish, da Abner ɗan Ner, da Yowab ɗan
Zeruhiya suka keɓe.
29 Daga mutanen Izhar,
Kenaniya da 'ya'yansa maza su aka sa a ayyukan da ba na haikali ba, su suka
zama manya da kuma alƙalai a bisa Isra'ila.
30 Daga zuriyar Hebron,
Hashabiya da danginsa, su jarumawa dubu ɗaya da ɗari bakwai ne, su suke
lura da Isra'ila yamma da Urdun don dukan aikin UBANGIJI da kuma hidimar
sarki. 31 Game da zuriyar Hebron kuwa, Yeriya ne babba bisa ga tarihin zuriyar
iyalansu.
A shekara ta arba'in ta sarautar Dawuda, sai aka yi binciken tarihi, aka tarar
jarumawa cikin zuriyar Hebron suna zama a Yazer cikin Gileyad ne. 32 Yeriya
yana da 'yan'uwa guda dubu biyu da ɗari bakwai, jarumawa da kuma
kawunan iyalai, sai Sarki Dawuda ya sa su lura da mutanen Ruben, Gad da
rabin kabilar Manasse game da kome da ya shafi Allah da kuma al'amuran
sarki.

# 27

*Ɓangarorin mayaƙa*

1 Wannan shi ne jerin Isra'ilawa, kawunan iyalai, shugabannin dubu-dubu
da shugabannin ɗari-ɗari, da manyan ma'aikatansu, waɗanda suka yi wa
sarki hidima a dukan abin da ya shafi ɓangarorin mayaƙan da suke aiki
wata-wata a dukan shekara. Kowane sashe yana da mutane 24,000.

2 Wanda yake lura da sashe na fari, na wata na farko, shi ne Yashobeyam ɗan
Zabdiyel. Akwai mutane 24,000 a sashensa. 3 Shi zuriyar Ferez ne kuma babba
na dukan shugabannin mayaƙa don wata na farko.
4 Wanda yake lura da sashen don wata na biyu shi ne Dodai mutumin Ahowa;
Miklot ne shugaban sashensa. Akwai mutane 24,000 a sashensa.

[†] **26:20** Seftuwajin; Ibraniyanci Game da Lawiyawa kuwa, Ahiya ne

5 Shugaban mayaƙa na uku, don wata na uku, shi ne Benahiya ɗan Yehohiyada
firist. Shi ne babba kuma akwai mutane 24,000 a sashensa. 6 Wannan shi ne
Benahiya wanda yake ɗaya daga cikin jarumawa Talatin nan kuma shi ne yake
babba a cikin Talatin ɗin. Ɗansa Ammizabad ne yake lura da sashensa.
7 Na huɗu, don wata na huɗu, shi ne Asahel ɗan'uwan Yowab; ɗansa Zebadiya shi ne magājinsa. Akwai mutane 24,000 a sashensa.
8 Na biyar don wata na biyar, shi ne Shamhut mutumin Izhar shugaban mayaƙa. Akwai mutane 24,000 a sashensa.
9 Na shida, don wata na shida, shi ne Ira ɗan Ikkesh mutumin Tekowa. Akwai mutane 24,000 a sashensa.
10 Na Bakwai, don wata na bakwai, shi ne Helez mutumin Felon, mutumin Efraim. Akwai mutane 24,000 a sashensa.
11 Na takwas, don wata na takwas, shi ne Sibbekai mutumin Husha, mutumin Zera. Akwai mutane 24,000 a sashensa.
12 Na tara, don wata na tara, shi ne Abiyezer mutumin Anatot, mutumin Benyamin. Akwai mutane 24,000 a sashensa.
13 Na goma, don wata na goma, shi ne Maharai mutumin Netofa, mutumin Zera. Akwai mutane 24,000 a sashensa.
14 Na goma sha ɗaya, don wata goma sha ɗaya, shi ne Benahiya mutumin Firaton, mutumin Efraim. Akwai mutane 24,000 a sashensa.
15 Na goma sha biyu don wata goma sha biyu, shi ne Heldai mutumin Netofa, daga iyalin Otniyel. Akwai mutane 24,000 a sashensa.

### *Manyan shugabannin Kabilu*

16 Shugabannin da suke bisa kabilan Isra'ila,

bisa mutanen Ruben su ne, Eliyezer ɗan Zikri;
bisa mutanen Simeyon shi ne, Shefatiya ɗan Ma'aka
17 bisa mutanen Lawi shi ne, Hashabiya ɗan Kemuwel;
bisa mutanen Haruna shi ne, Zadok;
18 bisa mutanen Yahuda shi ne, Elihu, ɗan'uwan Dawuda;
bisa mutanen Issakar shi ne, Omri ɗan Mika'ilu;
19 bisa mutanen Zebulun shi ne, Ishmahiya ɗan Obadiya;
bisa mutanen Naftali shi ne, Yerimot ɗan Azriyel;
20 bisa mutanen Efraim shi ne, Hosheya ɗan Azaziya;
bisa rabin kabilar Manasse shi ne, Yowel ɗan Fedahiya;
21 bisa ɗayan rabi kabilar Manasse a Gileyad shi ne, Iddo ɗan Zakariya;
bisa mutanen Benyamin shi ne, Ya'asiyel ɗan Abner;
22 bisa mutanen Dan shi ne, Azarel ɗan Yeroham.

Waɗannan su ne shugabanni a bisa kabilan Isra'ila.

23 Dawuda bai ƙirga mutanen da suke 'yan shekara ashirin ko ƙasa ba, domin
Ubangiji ya yi alkawari zai sa Isra'ila su yi yawa kamar taurari a sararin sama.
24 Yowab ɗan Zeruhiya ya fara ƙirgan mutanen amma bai gama ba. Hasala ta sauko a kan Isra'ila saboda wannan ƙirge, ba a kuma shigar da adadin a littafin tarihin Sarki Dawuda ba.

### *Masu lura da kayan sarki*

25 Azmawet ɗan Adiyel shi ne mai lura da ɗakuna ajiyar fada.
Yonatan ɗan Uzziya shi ne mai lura da ɗakunan ajiya a yankuna, cikin garuruwa, ƙauyuka da kuma hasumiyoyin tsaro.

26 Ezri ɗan Kelub shi ne mai lura da ma'aikatan gona waɗanda suke nome ƙasar.
27 Shimeyi mutumin Ramat shi ne mai lura da gonakin inabi.
Zabdi mutumin Shifam shi ne mai lura da amfanin gonakin inabi don matsin ruwan inabi.
28 Ba'al-Hanan mutumin Geder shi ne mai lura da itatuwan zaitun da na al'ul a gindin tuddan yamma.
Yowash shi ne mai lura da tanadin man zaitun.
29 Shitrai mutumin Sharon shi ne mai lura da garkuna masu kiwo a Sharon.
Shafat ɗan Adlai shi ne mai lura da garkuna a kwari.
30 Obil mutumin Ishmayel shi ne mai lura da raƙuma.
Yedehiya mutumin Meronot shi ne mai lura da jakuna.
31 Yaziz mutumin Hagiri shi ne mai lura da tumaki.
Dukan waɗannan shugabanni ne masu lura da mallakar Sarki Dawuda.

32 Yonatan, kawun Dawuda, shi ne mashawarci, mutum mai hangen nesa kuma marubuci.
Yehiyel ɗan Hakmoni ne ya lura da 'ya'yan sarki maza.
33 Ahitofel shi ne mashawarcin sarki.
Hushai mutumin Arkitawa shi ne abokin sarki na kud da kud.
34 Yehohiyada ɗan Benahiya da Abiyatar ne suka gāji Ahitofel.
Yowab shi ne shugaban mayaƙan masarauta.

# 28

*Shirye-shiryen Dawuda don haikali*

1 Dawuda ya sa aka kira dukan shugabannin Isra'ila su taru a Urushalima, shugabannin kabilu, manyan hafsoshin ɓangarorin hidimar sarki, manyan hafsoshin dubu-dubu da manyan hafsoshin ɗari-ɗari, da kuma shugabanni masu lura da dukan mallaka da dabbobin da suke na sarki da kuma 'ya'yansa maza, tare da fadawa, jarumawa da kuma dukan mayaƙa masu kwarjini.

2 Sarki Dawuda ya miƙe tsaye ya ce, "Ku saurare ni, 'yan'uwana da kuma mutanena. Na yi niyya in gina gida a matsayin wurin hutu domin akwatin alkawarin UBANGIJI, domin zatin Allahnmu, na kuma yi shiri don in gina shi.
3 Amma Allah ya ce mini, 'Ba za ka gina gida domin Sunana ba, saboda kai mayaƙi ne ka kuma zub da jini.'

4 "Duk da haka UBANGIJI, Allah na Isra'ila, ya zaɓe ni daga dukan iyalina don in zama sarki bisa Isra'ila har abada. Ya zaɓi Yahuda a matsayin shugaba, kuma daga gidan Yahuda ya zaɓi iyalina, daga 'ya'yan mahaifina maza kuwa ya gamsu ya mai da ni sarki bisa dukan Isra'ila.
5 Cikin dukan 'ya'yana maza, UBANGIJI kuwa ya ba ni su da yawa, ya zaɓi ɗana Solomon yă zauna a kujerar mulkin UBANGIJI a bisa Isra'ila.
6 Ya ce mini, 'Solomon ɗanka shi ne wanda zai gina gidana da filayen da suke kewaye da shi, gama na zaɓe shi yă zama ɗana, ni kuma zan zama mahaifinsa.
7 Zan kafa mulkinsa har abada in bai kauce ga kiyaye umarnaina da dokokina ba, yadda ake yi a wannan lokaci.'

8 "Saboda haka yanzu ina umartanku a gaban dukan Isra'ila da na taron jama'ar UBANGIJI, da kuma a kunnuwan Allahnmu. Ku yi hankali ku kiyaye dukan umarnan UBANGIJI Allahnku don ku mallaki wannan kyakkyawar ƙasa ku kuma bar wa zuriyarku gādo har abada.

9 "Kai kuma ɗana Solomon, ka san Allah na mahaifinka, ka kuma yi masa hidima da dukan zuciya da kuma yardar rai, gama UBANGIJI yana binciken zuciya, yana kuma gane dukan aniyar tunani. In ka neme shi, za ka same shi; amma in ka yashe shi,

zai ƙi ka har abada. 10 Ka lura fa, gama UBANGIJI ya zaɓe ka don ka gina haikali a
matsayin wuri mai tsarki. Ka yi ƙarfin hali ka kuma yi aiki."
11 Sa'an nan Dawuda ya ba ɗansa Solomon tsari domin shirayin haikalin, gine-
ginensa, ɗakunan ajiyarsa, ɓangarorin bisansa, ɗakunan cikinsa da kuma wurin
kafara. 12 Ya ba shi tsarin dukan abin da Ruhu ya sa a zuciyarsa saboda filayen
haikalin UBANGIJI da ɗakunan kewaye, da ma'ajin haikalin Allah da kuma baitulmali
na kayayyakin da aka keɓe. 13 Ya ba shi tsari game ɓangarori na firistoci da
Lawiyawa, da game dukan aikin hidima a cikin haikalin UBANGIJI, da kuma game da
dukan kayayyakin da za a yi amfani da su a hidima. 14 Ya kimanta yawan zinariya
don dukan kayayyakin zinariyar da za a yi amfani a kowane irin hidima, da yawan
azurfa don dukan kayayyakin azurfan da za a yi amfani a kowace irin hidima. 15 Da
yawan zinariya don wurin ajiye fitilan fitilu da fitilunsu, da yawan zinariyan da za
a yi amfani don kowace fitila da wurin ajiye fitilanta; da kuma yawan azurfa don
kowane wurin ajiye fitila da fitilunsa bisa ga yadda za a yi amfani da kowane wurin
ajiye fitila; 16 yawan zinariya don kowane tebur saboda burodi mai tsaki; da kuma
yawan azurfa saboda teburin azurfa; 17 yawan zinariya zalla, don cokula masu yatsu,
kwanonin yayyafawa ruwa da kuma tuluna; yawan zinariya don kowane kwanon
zinariya; yawan azurfa don kowane kwanon azurfa; 18 da kuma yawan tacecciyar
zinariya don bagaden turare. Ya kuma ba shi tsari don keken yaƙi, wato, kerubobin
zinariyar da suka miƙe fikafikansu suka inuwantar da akwatin alkawarin UBANGIJI.
19 Dawuda ya ce, "Dukan wannan, ina da shi a rubuce daga hannun UBANGIJI zuwa
gare ni, ya kuma ba ni ganewa cikin dukan tsarin fasalin, filla-filla."
20 Dawuda ya kuma ce wa Solomon ɗansa, "Ka yi ƙarfin hali, ka kuma yi aikin.
Kada ka ji tsoro ko ka fid da zuciya, gama UBANGIJI Allah, Allahna, yana tare da kai.
Ba zai bari ka ji kunya ko yǎ yashe ka ba, sai an gama dukan aikin saboda hidimar
haikalin UBANGIJI. 21 Sassan firistoci da na Lawiyawa suna a shirye domin dukan
aiki a haikalin Allah, kuma kowane gwani mai niyya a kowace sana'a, zai taimake
ka a cikin dukan aikin. Shugabanni da dukan mutane za su yi biyayya da kowane
umarninka."

# 29

*Kyautai don ginin haikali*

1 Sa'an nan Sarki Dawuda ya ce wa dukan taron, "Ɗana Solomon, wanda Allah ya
zaɓa, matashi ne, kuma bai gogu ba. Aikin yana da yawa, domin wannan ƙasaitaccen
ginin ba na mutum ba ne, na UBANGIJI Allah ne. 2 Na riga na tara dukan kayayyakin da
na tanada saboda haikalin Allahna, zinariya saboda dukan ayyukan zinariya, azurfa
saboda ayyukan azurfa, tagulla saboda ayyukan tagulla, ƙarfe saboda ayyukan ƙarfe
da kuma katako saboda ayyukan katako, da onis don ado, turkuwoyis, duwatsu
masu launi dabam-dabam, da kuma dukan duwatsu masu kyau da mabul, dukan
waɗannan suna nan jingim. 3 Ban da haka ma, cikin sa zuciyata ga haikalin Allahna,
yanzu na ba da ma'ajina na zinariya da azurfa saboda haikalin Allahna, fiye da kome
na tanada saboda wannan haikali, 4 talenti dubu uku na zinariya (zinariyar Ofir) da
tacecciyar azurfa dubu bakwai; don adon bangon gine-ginen, 5 don aikin zinariya da
kuma aikin azurfa, don kuma dukan aikin da gwanaye za su yi. Yanzu fa wa yake da
niyya yǎ miƙa kansa a yau don UBANGIJI?"
6 Sai shugabannin iyalai, shugabannin kabilan Isra'ila, manyan hafsoshin mayaƙa
dubu-dubu da manyan hafsoshi mayaƙa ɗari-ɗari, da shugabannin lura da ayyukan
sarki suka yi bayarwa da yardar rai. 7 Suka bayar talenti dubu biyar na zinariya,
talenti dubu goma na azurfa, talenti dubu goma sha takwas na tagulla da talenti dubu
ɗari na ƙarfe don aiki a haikalin Allah. 8 Duk waɗanda suke da duwatsu masu daraja

suka ba da su ga Yehiyel mutumin Gershon ma'ajin haikalin UBANGIJI. 9 Mutane suka
yi farin ciki ganin yadda shugabanninsu suke bayarwa da yardar rai, gama sun bayar
hannu sake da kuma dukan zuciya ga UBANGIJI. Dawuda sarki shi ma ya yi farin ciki
ƙwarai.

### *Addu'ar Dawuda*

10 Dawuda ya yabi UBANGIJI a gaban dukan taron, yana cewa,
"Yabo gare ka, ya UBANGIJI,
Allah na mahaifinmu Isra'ila,
har abada abadin.
11 Girma da iko
da ɗaukaka, da daraja da kuma nasara naka ne, ya UBANGIJI,
gama kome a sama da ƙasa naka ne.
Mulki kuma naka ne, ya UBANGIJI;
an kuma ɗaukaka ka a matsayin kai a bisa duka.
12 Wadata da girma daga gare ka suke;
kai ne mai mulkin dukan abubuwa.
A hannuwanka ne ƙarfi da iko suke
don ka ɗaukaka da kuma ba da ƙarfi ga duka.
13 Yanzu fa, Allahnmu, muna gode maka,
muna kuma yabon ɗaukakar sunanka.
14 "Amma wane ni, kuma wace ce jama'ata da za mu iya ba ka a yalwace kamar
haka? Kome daga gare ka suka fito, kuma mun ba ka abin da kawai ya fito daga
hannunka ne. 15 Mu bare ne kuma baƙi a gabanka, kamar yadda dukan kakanninmu
suke. Kwanakinmu a duniya suna kamar inuwa ne, ba sa zuciya. 16 Ya UBANGIJI
Allahnmu, game da dukan wannan yalwar da ka tanada saboda ginin haikali saboda
Sunanka Mai Tsarki, sun fito daga hannunka ne, kuma dukan naka ne. 17 Na
sani, Allahna, cewa kakan gwada zuciya, kakan kuma gamsu da mutunci. Dukan
waɗannan abubuwa na bayar da yardar rai da kuma kyakkyawar niyya. Yanzu
kuma da farin ciki na ga yadda mutanenka waɗanda suke a nan da yardar rai suka
ba ka. 18 Ya UBANGIJI Allah na kakanninmu Ibrahim, Ishaku da Isra'ila, ka sa wannan
sha'awa a cikin zukatan mutanenka har abada, ka kuma bar zukatansu su yi maka
biyayya. 19 Ka kuma ba ɗana Solomon cikakkiyar zuciya don yǎ kiyaye umarnanka,
farillanka da ƙa'idodinka yǎ kuma yi kome don yǎ gina ƙasaitaccen gini wanda na
riga na yi tanadi dominsa."
20 Sa'an nan Dawuda ya ce wa dukan taron, "Ku yabi UBANGIJI Allahnku." Saboda
haka suka yabi UBANGIJI Allah na kakanninsu; suka rusuna suka kuma fāɗi rubda
ciki a gaban UBANGIJI da kuma sarki.

### *An yarda da Solomon a matsayin sarki*

21 Kashegari suka miƙa hadayu ga UBANGIJI suka kuma miƙa hadayu bijimai dubu,
raguna dubu da kuma 'yan raguna dubu na ƙonawa gare shi, tare da hadayunsu na
sha da sauran hadayu a yalwace saboda dukan Isra'ila. 22 Suka ci suka sha da farin
ciki mai girma a gaban UBANGIJI a wannan rana.
Sa'an nan suka yarda da Solomon ɗan Dawuda a matsayin sarki sau na biyu, suka
shafe shi a gaban UBANGIJI don yǎ zama mai mulki, Zadok kuwa ya zama firist.
23 Saboda haka Solomon ya zauna a kujerar sarautar UBANGIJI a matsayin sarki a
maimakon mahaifinsa Dawuda. Ya yi nasara, dukan Isra'ila kuwa suka yi masa
biyayya. 24 Dukan shugabanni da jarumawa, har ma da dukan 'ya'yan Sarki Dawuda
maza, suka yi alkawari za su yi wa Sarki Solomon biyayya.
25 UBANGIJI ya ɗaukaka Solomon sosai a idon dukan Isra'ila, ya kuma ba shi darajar
sarauta yadda babu sarki a Isra'ilan da ya taɓa samu.

### *Mutuwar Dawuda*

26 Dawuda ɗan Yesse ya zama sarki a bisa dukan Isra'ila. 27 Ya yi mulki a bisa
Isra'ila shekaru arba'in, shekaru bakwai a Hebron da kuma shekaru talatin da uku
a Urushalima. 28 Ya mutu a kyakkyawar tsufa, bayan ya more dogon rai, wadata da
girma. Ɗansa Solomon ya gāje shi a matsayin sarki.
29 Game da ayyukan mulkin Sarki Dawuda, daga farko har ƙarshe, an rubuta su
a cikin tarihin Sama'ila mai duba, tarihin annabi Natan da kuma tarihin Gad mai
duba, 30 tare da yadda mulkinsa da ikonsa da yanayin da suka kewaye shi da Isra'ila
da kuma dukan masarautai na dukan sauran ƙasashe.

# 2 Tarihi

*Solomon ya nemi hikima*
*(1 Sarakuna 3.1-15)*

1 Solomon ɗan Dawuda ya kafa kansa sosai a bisa masarautarsa, gama UBANGIJI
Allahnsa yana tare da shi ya kuma sa ya zama mai girma sosai.

2 Sai Solomon ya yi magana ga dukan Isra'ila, ga shugabannin mayaƙa dubu-dubu
da shugabannin mayaƙa ɗari-ɗari, ga alƙalai da kuma ga dukan shugabanni a Isra'ila,
kawunan iyalai, 3 Solomon tare da dukan taron suka tafi masujadan kan tudu a
Gibeyon, gama Tentin Sujadar Allah yana can, wanda Musa bawan UBANGIJI ya yi a
hamada. 4 Dawuda ya riga ya haura da akwatin alkawarin Allah daga Kiriyat Yeyarim
zuwa inda ya shirya dominsa, domin yă kafa masa tenti a Urushalima. 5 Amma
bagaden tagullar da Bezalel ɗan Uri, ɗan Hur, ya yi a Gibeyon a gaba tabanakul na
UBANGIJI; saboda haka Solomon da taron suka neme nufin UBANGIJI a can. 6 Solomon
ya haura zuwa bagaden tagulla a gaban UBANGIJI a cikin Tentin Sujada, ya kuma miƙa
hadayu na ƙonawa dubbai a kansa.

7 A wannan dare Allah ya bayyana ga Solomon, ya ce masa, "Roƙi duk abin da kake
so in ba ka."

8 Solomon ya amsa wa Allah, "Ka nuna alheri mai girma ga Dawuda mahaifina ka
kuma naɗa ni sarki a matsayinsa. 9 To, yanzu, ya UBANGIJI Allah, ka cika alkawarin
da ka yi ga mahaifina Dawuda yă tabbata, gama ka naɗa ni sarki a bisa mutanen da
suka wuce ƙirge kamar ƙurar ƙasa. 10 Ka ba ni hikima da sani, don in iya jagorance
wannan mutane, gama wa zai iya shugabance wannan jama'arka mai girma?"

11 Allah ya ce wa Solomon, "Da yake wannan ne sha'awar zuciyarka, ba ka kuwa
nemi wadata, arziki ko girma ba, ba ka kuma nemi mutuwar abokan gābanka ba,
da yake kuma ba ka nemi tsawon rai ba, amma ka nemi hikima da sani don ka
shugabanci jama'ata wadda na naɗa ka sarki, 12 saboda haka za a ba ka hikima da
sani. Zan kuma ba ka wadata, arziki da girma, waɗanda babu wani sarki kafin kai
da ya taɓa kasance da su kuma babu wani a bayanka da zai kasance da su."

13 Sa'an nan Solomon ya tafi Urushalima daga masujadar kan tudu a Gibeyon, da
kuma daga gaban Tentin Sujada. Ya kuma yi mulki a bisa Isra'ila.

*(1 Sarakuna 10.26-29)*

14 Solomon ya tara kekunan yaƙi da dawakai, ya kasance da kekunan yaƙi dubu
da ɗari huɗu da kuma dawakai dubu goma sha biyu, waɗanda ya ajiye a biranen
kekunan yaƙi, da kuma tare da shi a Urushalima. 15 Sarki ya sa azurfa da zinariya
suka zama barkatai a Urushalima kamar duwatsu, al'ul kuma kamar itatuwan ﬁr
a gindin tsaunuka. 16 Aka shigo da dawakan Solomon daga Masar[*] da kuma daga
Kuye[†] 'yan kasuwan fada suka saye su daga Kuye. 17 Suka shigo da kekunan yaƙi
daga Masar a kan shekel ɗari shida-shida na azurfa, doki kuma a kan shekel ɗari da
hamsin-hamsin. Suka kuma riƙa fitar da su ƙasashen waje zuwa dukan sarakunan
Hittiyawa da na Arameyawa.

## 2

*Shirye-shirye don ginin haikali*
*(1 Sarakuna 5.1-12)*

[*] **1:16** Ko kuwa dai mai yiwuwa Muzur, wani yanki Silisiya; haka ma a aya 17. [†] **1:16** Wataƙila Silisiya.

1 Solomon ya ba da umarni don a gina haikali domin sunan Ubangiji da kuma fada
wa kansa. 2 Ya ɗebi mutane dubu saba'in su zama 'yan ɗauko, mutane dubu tamanin
su zama masu fasa dutse a tuddai, da kuma mutane dubu uku da ɗari shida su zama
masu lura da su.

3 Solomon ya aika wannan saƙo ga Hiram* sarkin Taya.

"Ka aika mini gumaguman al'ul kamar yadda ka yi wa mahaifina Dawuda sa'ad
da ka aika masa al'ul don yǎ gina fada yǎ zauna a ciki. 4 Yanzu ina shirin
ginin haikali domin Sunan Ubangiji Allahna, in kuma keɓe shi gare shi don ƙona
turare mai ƙanshi a gabansa, don kuma ajiyar burodi mai tsarki kullum, da
kuma don miƙa hadayun ƙonawa kowace safiya, kowace yamma, da a Asabbatai
da Sababbin Wata, da kuma a ƙayyadaddun bukukkuwan Ubangiji Allahnmu.
Wannan dawwammamiyar farilla ce don Isra'ila.

5 "Haikalin da zan gina zai zama mai girma, domin Allahnmu ya fi dukan sauran
alloli girma. 6 Amma wa zai iya gina haikali dominsa, shi wanda sammai, har ma
da sama sammai, ba za su iya riƙe shi ba? To, wane ne ni da zan gina haikali
dominsa, in ba dai wurin ƙona hadayu a gabansa ba?

7 "Saboda haka sai ka aiko mini da mutum wanda ya gwanince a aiki da azurfa,
tagulla, baƙin ƙarfe, da kuma shunayya, da garura, da shuɗɗan zare, da wanda
kuma ya gwanince da aikin sassaƙa, domin yǎ yi aiki tare da gwanayen mutane da
nake da su a Yahuda da Urushalima, waɗanda mahaifina Dawuda ya tanada.

8 "Ka kuma aika mini al'ul, fir da gumaguman algum daga Lebanon, gama na
san cewa mutanenka sun gwanince a yakan katakai a can. Mutanena kuwa za
su yi aiki tare da naka 9 don su tanada mini katakai da yawa, domin haikalin da
zan gina dole yǎ zama mai girma da kuma ƙasaitacce. 10 Zan ba wa bayinka
masu yankan katakai waɗanda suka yanka katako, garwa niƙaƙƙen alkama dubu
ashirin, garwan sha'ir dubu ashirin da randunan ruwan inabi dubu ashirin da
kuma randunan man zaitun dubu ashirin."

11 Hiram sarkin Taya ya amsa ta wurin rubuta wasiƙa zuwa ga Solomon.

"Domin Ubangiji yana ƙaunar mutanensa, ya naɗa ka sarkinsu."

12 Hiram ya ƙara da cewa,

"Yabo ga Ubangiji, Allah na Isra'ila, wanda ya yi sama da ƙasa! Ya ba Sarki
Dawuda ɗa mai hikima, cike da wayo da kuma sani, wanda zai gina haikali domin
Ubangiji da kuma fada wa kansa.

13 "Zan aika maka Huram-Abi, wani gwani wanda ya iya aiki, kuma mai hikima,
14 wanda mahaifiyarsa ta fito daga Dan, mahaifinsa kuma daga Taya. An horar
da shi a aikin zinariya, azurfa, tagulla, baƙin ƙarfe, dutse, itace, da kuma shuɗi,
shunayya, garura, da lilin mai kyau. Ya gogu a kowane irin zāne-zāne, zai kuma
iya yin kowane zānen da aka ba shi. Zai yi aiki tare da masu sana'arka, da kuma
tare da waɗanda ranka yǎ daɗe, Dawuda mahaifinka ya tanada.

15 "Yanzu fa, bari ranka yǎ daɗe, yǎ aiko wa bayinsa alkama da sha'ir da
kuma man zaitun da ruwan inabin da ka alkawarta, 16 za mu kuwa yanka dukan
gumagumai daga Lebanon da kake bukata za mu kuwa yi fitonsu ta teku, su gangara
zuwa Yaffa. Za ka iya kwashe su daga can ka haura zuwa Urushalima."

17 Solomon ya ƙidaya dukan baƙin da suke cikin Isra'ila, bayan ƙidayan da
mahaifinsa Dawuda ya yi; aka kuma tarar sun kai 153,600. 18 Ya sa 70,000 a cikinsu su
zama 'yan ɗauko, 80,000 kuma su zama masu fasan dutse a tuddai, sa'an nan 3,600
su zama shugabanni masu lura da aiki.

* **2:3** Da Ibraniyanci Huram, wani suna na Hiram; haka ma a ayoyi 11 da 12.

# 3

*Solomon ya gina haikali*
*(1 Sarakuna 6.1-38)*

1 Sai Solomon ya fara ginin haikalin UBANGIJI a Urushalima, a kan Dutsen Moriya,
inda UBANGIJI ya taɓa bayyana ga mahaifinsa Dawuda, inda kuma Dawuda ya riga
ya shirya a daidai masussukar Ornan mutumin Yebus. 2 Ya fara ginin a rana biyu ga
wata na biyu a shekara ta huɗu ta mulkinsa.
3 Tushen da Solomon ya kafa don ginin haikalin Allah tsawonsa kamun sittin,
fāɗinsa kamun ashirin ne (bisa ga tsohon ma'auni). 4 Shirayin da yake gaban haikalin
kuma kamun ashirin ne da ya nausa ya ƙetare, fāɗin ginin kuma tsayinsa kamu
ashirin ne.
Ya shafe cikin da zinariya zalla. 5 Ya shafe babban zauren da fir, ya kuma rufe
shi da zinariya mai kyau; ya yi masa ado da zāne-zānen itatuwan dabino da kuma
jerin zāne-zāne. 6 Ya yi wa haikalin ado da duwatsu masu daraja. Zinariyar
da ya yi amfani da su kuwa zinariya Farwayim ne. 7 Ya shafe ginshiƙan saman
ɗaki, madogaran ƙofofi, bangaye da kuma ƙofofin haikalin da zinariya, ya sassaƙa
kerubobi a bangayen.
8 Ya gina Wuri Mafi Tsarki, tsawonsa daidai da fāɗin haikalin. Tsawonsa kamu
ashirin, fāɗinsa kuwa kamu ashirin. Ya shafe cikin da talenti ɗari shida na zinariya
zalla. 9 Nauyin ƙusoshin ya kai shekel hamsin na zinariya. Ya kuma shafe benaye da
zinariya zalla.
10 Cikin Wuri Mafi Tsarki ya yi kerubobi biyu, ya kuma shafe su da zinariya.
11 Tsawon fikafikan kerubobin duka kamu ashirin ne, fiffike ɗaya, kamu biyar, ya
taɓo bangon ɗakin, ɗaya fiffiken kuma wanda shi ma kamu biyar ne, ya taɓo fiffiken
kerub ɗaya ɗin. 12 Haka ma fiffiken kerub na biyu ɗin tsawonsa kamu biyar ne, ya
taɓo bangon haikalin, ɗaya fiffiken shi ma tsawonsa kamu biyar ne, ya taɓo fiffiken
kerub na farko. 13 Tsawon fikafikan kerubobin ya kai kamu ashirin. Su kerubobin a
tsaye suke, suna fuskantar babban zauren.
14 Sai ya yi labule mai ruwan shuɗi, da shunayya, da garura, da lilin mai kyau, ya
kuma ƙunshi hotunan kerubobin da aka saƙa a cikinsa.

*(1 Sarakuna 7.15-22)*

15 A gaban haikalin ya yi ginshiƙai biyu, waɗanda tsawonsu ya kai kamu talatin
da biyar, ya yi wa ginshiƙan dajiya, tsayin kowace dajiya kamu biyar ne. 16 Ya saƙa
sarƙoƙi, ya kuma sa su a bisa ginshiƙan. Ya kuma yi rumman ɗari ya rataya wa
sarƙoƙin. 17 Ya kafa ginshiƙan a gaban haikalin, ɗaya a kudu, ɗaya kuma a arewa.
Ya kira wanda yake kudun, Yakin,* na arewan kuwa ya kira Bowaz.†

# 4

*Kayayyakin haikalin*
*(1 Sarakuna 7.23-51)*

1 Ya yi bagaden tagulla mai tsawo kamu ashirin, fāɗinsa kamu ashirin, tsayinsa
kuma kamu goma. 2 Ya yi ƙaton kwano mai suna Teku na zubin ƙarfe, mai siffar
da'ira, awonsa kamu goma ne daga da'ira zuwa da'ira tsayinsa kuma kamu biyar.
Ya ɗauki magwaji mai tsawo kamu talatin ya auna shi kewaye. 3 Kasa da da'ira
kuwa, akwai siffofin bijimai kewaye da ita, goma ga kowane kamu guda. An yi zubin
bijiman a jeri biyu a gefe guda na kwatarniya.
4 Tekun ya tsaya a kan bijimai goma sha biyu, uku na fuskantar arewa, uku na
fuskantar yamma, uku na fuskantar kudu, uku kuma na fuskantar gabas. Tekun ya

* **3:17** Yakin wataƙila yana nufin ya kahu. † **3:17** Bowaz wataƙila yana nufin a cikinsa akwai ƙarfi.

zauna a kansu, kuma ƙarfafun bayansu suna wajen tsakiya. 5 Kaurin ya kai tafin
hannu, kuma da'iransa ya yi kama da'irar kwaf, kama furen da ya tohu. Ya riƙe
randuna dubu uku.
6 Sa'an nan ya yi daruna goma don wanki ya sa biyar a gefen kudu, biyar kuma
a gefen arewa. A cikinsu kayan da za a yi amfani don ɗauraye hadayun ƙonawa,
amma firistoci suna amfani da ƙaton kwano mai suna Teku don wanki.
7 Ya yi wurin ajiye fitila goma na zinariya bisa ga tsari dominsu ya kuma sa su a
haikali, biyar a gefen kudu, biyar kuma a gefen arewa.
8 Ya yi tebur goma ya kuma sa su cikin haikalin, biyar a gefen kudu, biyar kuma a
gefen arewa. Ya kuma yi kwanonin yayyafawa guda ɗari.
9 Ya yi fili na firistoci da kuma babban fili da ƙofofi domin filin, ya shafe ƙofofin
da tagulla. 10 Ya sa ƙaton kwano mai suna Teku a gefen kudu, a kusurwa kudu maso
gabas.
11 Ya kuma yi tukwane da manyan cokula da kwanonin yayyafawa.
Ta haka Huram ya gama aikin da ya yi wa Sarki Solomon a cikin haikalin Allah.

12 Ginshiƙai biyu;
kwanoni biyu masu siffar kwartaniya a bisa ginshiƙai;
jeri biyu na tuƙaƙƙen adon kwanonin yayyafawa masu siffar kwartaniya a bisa ginshiƙai;
13 rumman ɗari huɗu don jeri biyu na tuƙaƙƙe (layi biyu na rumman don kowane tuƙaƙƙe, mai adon kwano mai siffar kwartaniya a bisan ginshiƙai);
14 dakalai da darunansu;
15 ya yi kwanon da ya kira Teku, da bijimai goma sha biyu a ƙarƙashinsa;
16 tukwane, manyan cokula, cokula masu yatsu don nama da dukan kayayyakin da suka shafi wannan.

Dukan kayayyakin da Huram-Abi ya yi domin Sarki Solomon saboda haikalin
UBANGIJI an yi su da gogaggen tagulla ne. 17 Sarki ya sa aka yi zubinsu a katakon
yin tubali a filin Urdun tsakanin Sukkot da Zereda. 18 Dukan waɗannan abubuwa da
Solomon ya yi suna da tsada ƙwarai har suka kai nauyin tagullar da ya fi misali.
19 Solomon ya kuma yi dukan kayayyakin da suke a cikin haikalin Allah.

Bagaden zinariya;
teburin da ake ajiye burodin Kasancewa;
20 wurin ajiye fitila na zinariya zalla tare da fitilunsu, don ƙonawa a gaban wuri mai tsarki na ciki kamar yadda aka tsara;
21 aikin zānen furannin zinariya da fitilu da abin ɗiban wuta (an yi su da zinariya zalla);
22 arautaki; kwanonin yayyafawa, kwanoni da hantsuka; da kuma ƙofofin zinariya na haikali, ƙofofi na ciki zuwa Wuri Mafi Tsarki da kuma ƙofofin babban zaure.

# 5

1 Sa'ad da dukan aikin da Solomon ya yi domin haikalin UBANGIJI ya gama, sai ya
kawo abubuwan da mahaifinsa Dawuda ya keɓe a ciki, azurfa da zinariya da kuma
dukan kayayyaki, ya kuwa sa su a cikin ma'ajin haikalin Allah.

### *An kawo akwatin alkawari a haikali*
*(1 Sarakuna 8.1-13)*

2 Sa'an nan Solomon ya tattara zuwa Urushalima dattawan Isra'ila, dukan kawunan
kabilu da manyan iyalan Isra'ilawa, don su haura da akwatin alkawarin UBANGIJI

daga Sihiyona, Birnin Dawuda. 3 Dukan mutanen Isra'ila kuwa suka tattaru gaba
ɗaya suka zo wurin sarki a lokacin biki a wata na bakwai.

4 Sa'ad da dukan dattawan Isra'ila suka iso, Lawiyawa suka ɗauki akwatin
alkawarin, 5 suka haura da akwatin alkawarin da kuma Tentin Sujada da dukan
kayayyaki masu tsarkin da yake cikinta. Firistoci, waɗanda suke Lawiyawa, suka
ɗauke su; 6 Sarki Solomon kuwa da taron Isra'ila gaba ɗaya da suka taru kewaye da
shi suna a gaban akwatin alkawarin, suna miƙa tumaki da shanu masu yawa da suka
wuce ƙirge ko lissafi.

7 Sa'an nan firistoci suka kawo akwatin alkawarin Ubangiji zuwa wurinsa a ciki
cikin wuri mai tsarki na haikali, Wuri Mafi Tsarki, suka sa shi ƙarƙashin fikafikan
kerubobin. 8 Kerubobin suka buɗe fikafikansu a bisa wurin akwatin alkawari suka
kuma rufe akwatin alkawarin da sandunan ɗaukonsa. 9 Waɗannan sanduna sun yi
tsawo ƙwarai har ƙarshensu sun nausa daga akwatin alkawarin, ana iya ganinsu
daga gaban ciki wuri mai tsarki na can ciki amma ba daga waje Wuri Mai Tsarki
ba; kuma suna nan a can har wa yau. 10 Babu wani abu a cikin akwatin alkawarin
sai alluna biyu da Musa ya sa a cikinsa a Horeb, inda Ubangiji ya yi alkawari da
Isra'ilawa bayan sun fito Masar.

11 Sa'an nan firistoci suka janye daga Wuri Mai Tsarki. Dukan firistocin da suke can
sun tsarkake kansu, ko daga wace ɓangarori suka fito. 12 Dukan Lawiyawa waɗanda
suke mawaƙa, Asaf, Heman, Yedutun da 'ya'yansu maza da dangoginsu, suka tsaya a
gefen gabas na bagaden, saye da lilin mai kyau suna kuma kaɗa ganguna, garayu da
molaye. Tare da su akwai firistoci 120 masu busan ƙahoni. 13 Masu busan ƙahonin
da mawaƙa suka haɗu da baki ɗaya sai ka ce murya guda ce, don su yabi su kuma
yi godiya ga Ubangiji. Haɗe da busan ƙahoni, ganguna da sauran kayayyaki, suka tā
da muryoyinsu cikin yabo ga Ubangiji suka rera,

"Yana da kyau;
ƙaunarsa dawwammamiya ce har abada."

Sai haikalin Ubangiji ya cika da girgije, 14 Firistoci ba su iya yin hidimarsu ba
saboda girgijen, gama ɗaukakar Ubangiji ta cika haikalin Allah.

# 6

1 Sa'an nan Solomon ya ce, "Ubangiji ya faɗa cewa zai zauna cikin duhun girgije;
2 na gina ƙasaitaccen haikali dominka, wuri domin ka zauna har abada."

*(1 Sarakuna 8.14-21)*

3 Yayinda dukan taron Isra'ila suke tsaye a can, sai sarki ya juya ya albarkace su.
4 Sa'an nan ya ce,

"Yabo ya tabbata ga Ubangiji, Allah na Isra'ila, wanda da hannuwansa ya cika
abin da ya yi alkawari da bakinsa ga mahaifina Dawuda. Gama ya ce, 5 'Tun ranar
na da fitar da mutanena daga Masar, ban zaɓi wani birni a wata kabilar Isra'ila
don a gina haikali domin Sunana ya kasance a can ba, ba kuwa zaɓi wani yă zama
shugaba a bisa jama'ata Isra'ila ba. 6 Amma yanzu na zaɓi Urushalima domin
Sunana yă kasance a can, na kuma zaɓi Dawuda yă yi mulkin mutanena Isra'ila.'

7 "Mahaifina Dawuda ya yi niyya a zuciyarsa yă gina haikali domin Sunan
Ubangiji, Allah na Isra'ila. 8 Amma Ubangiji ya ce wa mahaifina Dawuda, 'Domin
yana a zuciyarka ka gina haikali domin Sunana, ka yi daidai da ka kasance da
wannan a zuciyarka. 9 Duk da haka, ba kai ba ne za ka gina haikalin, amma ɗanka
wanda yake namanka da jininka, shi ne wanda zai gina haikali domin Sunana.'

10 "Ubangiji ya kiyaye alkawarin da ya yi. Na gāje Dawuda mahaifina yanzu kuwa
na zauna a kan kujerar sarautar Isra'ila, kamar dai yadda Ubangiji ya alkawarta,

na kuma gina haikali domin Sunan Ubangiji, Allah na Isra'ila. 11 A can na ajiye
akwatin alkawari, inda alkawarin Ubangiji da ya yi da mutanen Isra'ila yake."

### *Addu'ar Solomon ta keɓewa*
### *(1 Sarakuna 8.22-53)*

12 Sa'an nan Solomon ya tsaya a gaban bagaden Ubangiji a gaban dukan taron
Isra'ila ya ɗaga hannuwansa sama. 13 Dā ma ya riga ya gina dakalin tagulla, mai
tsawo kamu biyar, fāɗi kamu biyar da kuma tsayi kamu uku, ya kuma sa shi a tsakiyar
filin waje. Ya tsaya a kan dakalin ya kuma durƙusa a gaban dukan taron Isra'ila ya
buɗe hannuwansa sama. 14 Ya ce,
"Ya Ubangiji, Allah na Isra'ila, babu Allah kamar ka a sama da kuma ƙasa, kai
da kake kiyaye alkawarinka na ƙauna tare da bayinka waɗanda suke cin gaba da
zuciya ɗaya a hanyarka. 15 Ka kiyaye alkawarinka ga bawanka Dawuda mahaifina;
da bakinka ka yi alkawari kuma da hannunka ka cika shi, yadda yake a yau.
16 "Yanzu fa Ubangiji, Allah na Isra'ila, ka kiyaye wa bawanka Dawuda mahaifina
alkawuran da ka yi masa sa'ad da ka ce, 'Ba za ka kāsa kasance da mutumin da
zai zauna a gabana a kan kujerar sarautar Isra'ila ba, in kawai 'ya'yanka maza za
su kula cikin dukan abin da suke yi su yi tafiya a gabana bisa ga dokata, kamar
yadda ka yi.' 17 Yanzu kuwa, ya Ubangiji, Allah na Isra'ila, bari maganarka da ka
yi alkawarta wa bawanka Dawuda yǎ cika.
18 "Amma tabbatacce Allah zai zauna a duniya tare da mutane? Sammai, har
ma da saman sammai, ba za su iya riƙe ka ba. Balle wannan haikalin da na gina!
19 Duk da haka ka mai da hankali ga addu'ar bawanka da kuma roƙo don jinƙai,
ya Ubangiji, Allahna. Ka ji kuka da addu'ar da bawanka yake yi a gabanka. 20 Bari
idanunka su buɗu ta wajen wannan haikali dare da rana, wannan wurin da ka ce
za ka sa Sunanka a can. Bari ka ji addu'ar da bawanka ke yi ta wajen wannan wuri.
21 Ka ji roƙe-roƙen bawanka da na mutanenka Isra'ila sa'ad da suka yi addu'a suna
duban wajen wannan wuri. Ka ji daga sama, mazauninka; kuma sa'ad da ka ji, ka
gafarta.
22 "Sa'ad da mutum ya yi wa maƙwabcinsa laifi aka kuma bukaci ya yi rantsuwa,
ya kuma zo ya rantse a gaban bagadenka a cikin wannan haikali, 23 sai ka ji daga
sama ka kuma yi wani abu. Ka shari'anta tsakanin bayinka, kana sāka wa mai laifi
ta wurin kawo a kansa hakkin abin da ya yi. Ka nuna cewa marar laifi ba shi da
laifi, ta haka a fiffita rashin laifinsa.
24 "Sa'ad da an ci mutanenka Isra'ila a yaƙi ta wurin abokin gāba domin sun yi
maka zunubi kuma sa'ad da suka juya suka furta sunanka, suna addu'a suka kuma
yin roƙe-roƙe a gabanka a wannan haikali, 25 sai ka ji daga sama ka kuma gafarta
zunubin mutanenka Isra'ila ka kuma dawo da su zuwa ƙasar da ka ba su da kuma
kakanninsu.
26 "Sa'ad da sammai suka rufu ba kuwa ruwan sama saboda mutanenka sun yi
maka zunubi, sa'ad da kuwa suka yi addu'a suna duban waje wannan wuri suka
kuma furta sunanka suka juye daga zunubinsu domin ka azabta su, 27 sai ka ji daga
sama ka kuma gafarta zunubin bayinka, mutanenka Isra'ila. Ka koya musu hanyar
da ta dace da za su yi zama, ka kuma aika ruwan sama a ƙasar da ka ba mutanenka
gādo.
28 "Sa'ad da yunwa ko annoba ta fāɗo a ƙasar, ko wahala ko fumfuna, ko fāra
ko fāra ɗango, ko sa'ad da abokan gāba sun yi musu ƙawanya a kowane daga
biranensu, dukan wata masifa ko cutar da za tǎ zo, 29 sa'ad da kuwa wani cikin
mutanenka Isra'ila ya yi wata addu'a ko roƙo, kowa yana sane a azabarsa da kuma
zafinsa, yana buɗe hannuwansa yana duban wajen wannan haikali, 30 sai ka ji daga
sama, mazauninka. Ka gafarta, ka kuma yi da kowane mutum gwargwadon duk

abin da yake yi, da yake ka san zuciyarsa (gama kai kaɗai ka san zukatan mutane),
31 don su ji tsoronka su kuma yi tafiya a hanyoyinka a kowane lokacin da suke
zama a ƙasar da ka ba wa kakanninsu.
32 “Game da baƙo wanda shi ba na mutanenka Isra’ila ba kuwa amma ya zo daga
ƙasa mai nisa saboda sunanka mai girma da kuma hannunka mai iko da hannunka
mai ƙarfi, sa’ad da ya zo ya yi addu’a yana duban wannan haikali, 33 sai ka ji daga
sama, mazauninka, ka kuma yi duk abin da baƙon ya nemi ka yi, saboda dukan
mutanen duniya su san sunanka su kuma ji tsoronka, kamar yadda mutanenka
Isra’ila suke yi, su kuma san cewa wannan gidan da na gina na Sunanka ne.
34 “Sa’ad da mutanenka suka je yaƙi da abokan gābansu, ko’ina ka kai su, kuma
sa’ad da suka yi addu’a gare ka suna duban wannan birnin da ka zaɓa da haikalin
nan da na gina domin Sunanka, 35 sai ka ji addu’arsu da kuma roƙonsu daga sama,
ka kuma biya musu bukatarsu.
36 “Sa’ad da suka yi maka zunubi, gama babu wani wanda ba ya zunubi, ka kuwa
yi fushi da su ka miƙa su ga abokin gāba, wanda ya kai su zaman bauta a ƙasa
mai nisa ko kuwa kusa; 37 Kuma in suka canja zuciya a cikin ƙasar da suke zaman
bauta, suka tuba suka roƙe ka a ƙasar zaman bautarsu suka kuma ce, ‘Mun yi
zunubi, mu yi abin da ba daidai ba, mu kuwa yi mugunta’; 38 in kuma sun juye
gare ka da dukan zuciyarsu da ransu a ƙasar zaman bautarsu inda aka kai su, suka
kuma dubi wajen ƙasar da ka ba wa kakanninsu, wajen birnin da ka zaɓa da kuma
wajen haikalin da na gina domin Sunanka; 39 to, daga sama, mazauninka, sai ka ji
addu’arsu da kuma roƙe-roƙensu, ka kuwa biya musu bukatunsu. Ka gafarta wa
mutanenka, waɗanda suka yi maka zunubi.
40 “Yanzu, Allahna, bari idanunka su buɗu kunnuwanka kuma su saurara ga
addu’o’in da ake miƙa a wannan wuri.

41 “Yanzu ka tashi, ya Ubangiji Allah, ka zo wurin hutunka,
kai da akwatin alkawarin ƙarfinka.
Bari firistocinka, ya Ubangiji Allah, su sanye ceto,
bari tsarkakanka su yi farin ciki cikin alherinka.
42 Ya Ubangiji Allah, kada ka ƙyale shafaffenka.
Ka tuna da ƙauna mai girma da ka alkawarta wa Dawuda bawanka.”

# 7

### *Keɓewar haikali*
### *(1 Sarakuna 8.62-66)*

1 Sa’ad da Solomon ya gama yin addu’a, sai wuta ya sauko daga sama ya cinye
hadaya ta ƙonawa da kuma sadakokin, ɗaukakar Ubangiji kuwa ta cika haikalin.
2 Firistoci ba su iya shiga haikalin Ubangiji ba domin ɗaukakar Ubangiji ta cika shi.
3 Sa’ad da dukan Isra’ilawa suka ga wutar na saukowa, ɗaukakar Ubangiji kuma tana
a bisa haikalin, sai suka durƙusa a dakali da fuskokinsu a ƙasa, suka yi sujada suka
kuma yi godiya ga Ubangiji suna cewa,

“Ubangiji mai alheri ne,
ƙaunarsa dawwammamiya ce har abada.”

4 Sai sarki da dukan mutanen suka miƙa hadayu a gaban Ubangiji. 5 Sarki Solomon
kuwa ya miƙa hadayar bijimai dubu ashirin da biyu da kuma tumaki da awaki dubu
ɗari da dubu ashirin. Ta haka sarki da dukan mutane suka keɓe haikalin Allah.
6 Firistoci suka ɗauki matsayinsu, haka kuma Lawiyawa suka tsaya a matsayinsu riƙe
da kayansu na bushe-bushe da na kaɗe-kaɗe na Ubangiji, waɗanda Sarki Dawuda
ya yi domin yabon Ubangiji. An yi amfani da su sa’ad da ake godiya, ana kuma
cewa, “Kaunarsa dawwammamiya ce har abada.” Kurkusa da Lawiyawa, firistoci
suka busa ƙahoninsu, dukan Isra’ila kuwa suna a tsaye.

7 Solomon ya tsarkake sashen tsakiya na filin da yake gaban haikalin UBANGIJI, a
can ya miƙa hadayun ƙonawa da kitsen hadayun salama domin bagaden tagullar
da ya yi ba zai iya ɗaukan hadayun ƙonawa, hadayun hatsi da kuma ɓangarori na
kitsen ba.
8 Ta haka Solomon ya kiyaye bikin a wannan lokaci har kwana bakwai, dukan
Isra'ila kuwa tare da shi, babban taro, mutane daga Lebo Hamat har zuwa Rafin
Masar. 9 A rana ta takwas sai suka yi taro, gama sun yi bikin keɓewar bagade na
kwana bakwai da kuma biki na ƙarin kwana bakwai. 10 A rana ta ashirin da uku na
watan bakwai sai ya sallami mutane su tafi gidajensu da farin ciki da kuma murna
a zuciya saboda abubuwa masu kyau da UBANGIJI ya yi domin Dawuda da Solomon
da kuma domin mutanensa Isra'ila.

### *UBANGIJI ya bayyana ga Solomon (1 Sarakuna 9.1-9)*

11 Sa'ad da Solomon ya gama haikalin UBANGIJI da kuma fadan sarki ya kuma yi
nasara a yin dukan abin da yake a zuciyarsa da zai yi a haikalin UBANGIJI da kuma a
fadarsa, 12 sai UBANGIJI ya bayyana gare shi a daren ya ce,

"Na ji addu'arka na kuma zaɓi wannan wuri don kaina, a matsayin haikali don hadayu.

13 "Sa'ad da na kulle sammai don kada a yi ruwan sama ko na umarci fāri su
cinye amfanin ƙasar ko kuwa na aika da annoba a cikin mutanena, 14 in mutanena,
waɗanda ake kira da sunana, sun ƙasƙantar da kansu, suka kuma yi addu'a, suka
nemi fuskata, suka kuma juye daga mugayen hanyoyinsu, zan ji daga sama in kuma
gafarta zunubinsu in kuwa warkar da ƙasarsu. 15 Yanzu, idanuna za su buɗu,
kunnuwata kuma za su saurara ga addu'o'in da aka miƙa a wannan wuri. 16 Na
zaɓi na kuma tsarkake wannan haikali saboda Sunana yă kasance a can har abada.
Idanuna da kuma zuciyata kullum za su kasance a can.
17 "Game da kai kuwa, in ka yi tafiya a gabana kamar yadda Dawuda mahaifinka
ya yi, ka kuma yi dukan abin da na umarta, ka kiyaye ƙa'idodina da dokokina,
18 zan kafa kujerar sarautarka, yadda na alkawarta wa Dawuda mahaifinka sa'ad
da na ce, 'Ba za ka taɓa rasa wani mutumin da zai yi mulki a bisa Isra'ila ba.'
19 "Amma in ka juya daga gare ni ka yashe ƙa'idodi da umarnan da na ba ka, ka
yi gaban kanka don ka bauta wa waɗansu alloli ka kuma yi musu sujada, 20 zan
tumɓuke Isra'ila daga ƙasata, wadda na ba su, zan kuma ƙi wannan haikalin da
na tsarkake domin Sunana. Zan mai da shi abin karin magana da abin ba'a cikin
dukan mutane. 21 Ko da yake wannan haikali yanzu mai girma ne, dukan wanda ya
wuce zai kaɗa kai yă ce, 'Me ya sa UBANGIJI ya yi irin wannan abu ga wannan ƙasa
da kuma ga wannan haikali?' 22 Mutane za su amsa, 'Domin sun yashe UBANGIJI
Allah na kakanninsu, wanda ya fitar da su daga Masar, suka rungumi waɗansu
alloli, suna musu sujada, suna bauta musu, shi ya sa ya kawo dukan wannan masifa
a kansu.' "

# 8

### *Sauran ayyukan Solomon (1 Sarakuna 9.10-28)*

1 A ƙarshen shekaru ashirin, a lokacin da Solomon ya gina haikalin UBANGIJI da
nasa fadan, 2 Solomon ya sāke gina ƙauyukan da Hiram ya ba shi, ya kuma zaunar
da Isra'ilawa a cikinsu. 3 Sa'an nan Solomon ya tafi Hamat-Zoba ya ci ta da yaƙi. 4 Ya
kuma gina Tadmor a hamada da kuma dukan biranen ajiyar da ya gina a Hamat. 5 Ya
sāke gina Bet-Horon na Bisa da kuma Bet-Horon na Kasa a matsayin birane masu
katanga, da bangaye da ƙofofi da kuma ƙyamare, 6 haka kuma Ba'alat da dukan

biranen ajiyarsa, da kuma dukan birane domin keken yaƙinsa da dawakansa, duk
abin da ya so yă gina a Urushalima, a Lebanon da kuma dukan yankin da ya yi mulki,
ya gina shi.
[7] Dukan mutanen da suka rage daga Hittiyawa, Amoriyawa, Ferizziyawa, Hiwiyawa
da Yebusiyawa (waɗannan mutane ba Isra'ilawa ba ne), [8] wato, zuriyarsu da suka
ragu a ƙasar, wadda Isra'ilawa ba su hallaka ba, waɗannan ne Solomon ya mai
da su bayinsa na aikin dole, kamar yadda yake har wa yau. [9] Amma Solomon bai
mai da Isra'ilawa bayi don aikinsa ba; su ne mayaƙansa, shugabannin hafsoshinsa,
da shugabannin keken yaƙinsa da kuma mahayan keken yaƙinsa. [10] Su ne kuma
manyan ma'aikatan Sarki Solomon, manyan mutane ɗari biyu da hamsin masu lura
da mutane.
[11] Solomon ya kawo 'yar Fir'auna daga Birnin Dawuda zuwa fadan da ya gina
mata, gama ya ce, "Matata ba za tă zauna a fadan Dawuda sarkin Isra'ila ba, domin
wuraren da akwatin alkawarin UBANGIJI ya shiga masu tsarki ne."
[12] A kan bagaden UBANGIJI da ya gina a gaban shirayi, Solomon ya miƙa hadayun
ƙonawa ga UBANGIJI, [13] bisa ga bukace-bukace na kullum don hadayun da Musa
ya umarta don Asabbatai, Sabon Wata da kuma bukukkuwa uku na shekara, Bikin
Burodi Marar Yisti, Bikin Makoni da Bikin Tabanakul. [14] Bisa ga farillar mahaifinsa
Dawuda, ya naɗa ɓangarori na firistoci don ayyukansu da Lawiyawa don su jagoranci
yabo su kuma taimaki firistoci bisa ga bukace-bukacen kowace rana. Ya kuma naɗa
matsara ƙofofi ɓangarori, ɓangarori don ƙofofi dabam-dabam domin abin da Dawuda
mutumin Allah ya umarta ke nan. [15] Ba a kuwa yi rashin biyayya ba game da abin
da sarki ya umarta game da firistoci ko Lawiyawa a kan kayan haikalin ba.
[16] An yi dukan ayyukan Solomon, daga ranar kafa tushen haikalin UBANGIJI har
gamawarsa. Ta haka aka gama haikalin UBANGIJI.
[17] Sa'an nan Solomon ya tafi Eziyon Geber da Elot a bakin tekun Edom. [18] Sai
Hiram ya aika masa jiragen ruwan da masu tuƙinsu waɗanda suka san teku sosai.
Ma'aikatan Hiram suka tafi da na Solomon zuwa Ofir suka dawo da talentin zinariya
ɗari huɗu da hamsin wa Sarki Solomon.

# 9

*Sarauniyar Sheba ta ziyarci Solomon*
*(1 Sarakuna 10.1-13)*

[1] Sa'ad da sarauniyar Sheba ta ji shahararr Solomon, sai ta zo Urushalima tă gwada
shi da tambayoyi masu wuya. Ta iso tare da ayari mai girma, da raƙuma ɗauke da
kayan yaji, zinariya mai yawa, da kuma duwatsu masu daraja, ta zo wurin Solomon
ta kuma yi magana da shi game da dukan abin da yake zuciyarta. [2] Solomon ya
amsa dukan tambayoyinta; babu wani abin da ya yi masa wuya yă bayyana mata.
[3] Sa'ad da sarauniyar Sheba ta ga hikimar Solomon da kuma fadan da ya gina, [4] ta ga
abincin da yake teburinsa, ta ga zaman fadawansa, bayi masu yin masa hidima cikin
rigunansu, ta ga masu riƙe kwaf cikin rigunansu da kuma hadayun ƙonawar da ya
yi a haikalin UBANGIJI, sai mamaki ya kama ta.
[5] Ta ce wa sarki, "Labarin da na ji a ƙasata game da nasarorinka da hikimarka,
gaskiya ne. [6] Amma ban gaskata abin da suka faɗa ba sai da na zo na kuma gani
da idanuna. Tabbatacce, ko rabin girman hikimarka ba a faɗa mini ba, ka wuce
labarin da na ji nesa ba kusa ba. [7] Abin farin ciki ne ga mutanenka! Abin farin
ciki ne ga fadawanka, waɗanda suke cin gaba da tsayawa a gabanka suna kuma jin
hikimarka! [8] Yabo ya tabbata ga UBANGIJI Allahnka, wanda ya ji daɗi a cikinka ya
sa ka a kan kujerar sarautarsa a matsayin sarki don ka yi mulkin domin UBANGIJI

Allahnka. Saboda ƙaunar Allahnka wa Isra'ila da kuma sha'awarsa na riƙe su har abada, ya naɗa ka sarki a bisansu, don ka yi adalci da kuma gaskiya."
9 Sa'an nan ta ba sarki talenti 120 na zinariya, kayan yaji masu yawa, da kuma duwatsu masu daraja. Ba a taɓa kasance da irin kayan yaji mai yawa kamar waɗanda sarauniyar Sheba ta ba wa sarki Solomon ba.
10 (Mutanen Hiram da mutanen Solomon suka kawo zinariya daga Ofir, suka kuma kawo gungumen algum da duwatsu masu daraja. 11 Sarki ya yi amfani da gungumen algum don matakalan haikalin UBANGIJI da kuma na fadan sarki, ya kuma yi garayu da molaye don mawaƙa. Ba a taɓa gani irinsu a Yahuda ba.)

*(1 Sarakuna 10.14-29)*

12 Sarki Solomon ya ba sarauniyar Sheba duk abin da take so da kuma ta nema; ya ba ta fiye da abin da ta kawo masa. Sa'an nan ta tashi ta koma ƙasarta tare da masu rufe mata baya.

### *Ɗaukakar Solomon*

13 Nauyin zinariyar da Solomon yake karɓa shekara-shekara talenti 666 ne, 14 ban
da harajin da fatakai da 'yan kasuwa suke biya. Haka kuma dukan sarakunan Arabiya da gwamnonin ƙasar suka kawo zinariya da azurfa wa Solomon.
15 Sarki Solomon ya yi manyan garkuwoyi ɗari biyu da zinariya; an yi kowane garkuwa da bekas ɗari shida na zinariya. 16 Ya kuma yi ƙanana garkuwoyi zinariya ɗari uku, da bekas ɗari uku na zinariya a kowanne. Sarki ya sa su a cikin Fadan da ake kira Kurmin Lebanon.
17 Sai sarki ya yi wata kujerar sarauta mai girma da aka shafe ta da hauren giwa, aka kuma dalaye ta da zinariya zalla. 18 Kujerar tana da matakalai shida, da wurin sa ƙafa na zinariya haɗe da ita. A kowane gefen wurin zama, akwai wurin ajiye hannu, da zaki tsaye kusa da kowannensu. 19 Zakoki goma sha biyu sun tsaya a kan matakalai shida, ɗaya a ƙarshen matakala guda. Ba a taɓa yin irin wannan abu don wata masarauta ba. 20 Dukan kwaf na Sarki Solomon zinariya ne, kuma dukan kayayyakin gida a Fadan da ake kira Kurmin Lebanon zinariya ne zalla. Ba a yi wani abu da azurfa ba, domin ba a ɗauki azurfa a zamanin Solomon a bakin kome ba.
21 Sarki yana da jerin jiragen ruwa na kasuwanci waɗanda mutanen Hiram ne suke kula da su. Sau ɗaya kowace shekara uku sukan dawo ɗauke da zinariya, azurfa, hauren giwa, gogo da kuma birai.
22 Sarki Solomon ya fi arziki da hikima in aka kwatanta da dukan sauran sarakunan duniya. 23 Dukan sarakunan duniya sun nemi su sadu da Solomon don su ji hikimar da Allah ya sa a zuciyarsa. 24 Shekara, shekara, duk wanda ya zo wurinsa yakan kawo kyauta, kayayyakin azurfa da na zinariya, da riguna, makamai da kayan yaji, da dawakai da kuma alfadarai.
25 Solomon ya kasance da wuraren ajiye dawakai dubu huɗu don dawakai da kekunan yaƙi, yana da dawakai dubu goma sha biyu waɗanda ya ajiye a biranen kekunan yaƙi da kuma tare da shi a Urushalima. 26 Ya yi mulki bisa dukan sarakuna daga Kogi Yuferites zuwa ƙasar Filistiyawa, har zuwa iyakar Masar. 27 Sarki ya sa azurfa ta zama barkatai a Urushalima kamar duwatsu, al'ul kuma da yawa kamar itatuwan fir a gindin tsaunuka. 28 An sayo dawakan Solomon daga Masar da kuma daga dukan sauran ƙasashe.

### *Mutuwar Solomon*

*(1 Sarakuna 11.41-43)*

29 Game da sauran ayyukan mulkin Solomon, daga farko har zuwa ƙarshe, an rubuta su a cikin tarihin annabi Natan, cikin annabcin Ahiya mutumin Shilo da kuma cikin wahayin Iddo mai gani game da Yerobowam ɗan Nebat. 30 Solomon ya yi mulki
a Urushalima a bisa dukan Isra'ila shekaru arba'in. 31 Sa'an nan ya huta tare da

kakanninsa, aka kuma binne shi cikin birnin Dawuda mahaifinsa. Rehobowam ɗansa kuwa ya gāje shi a matsayin sarki.

# 10

*Isra'ila ya yi tawaye a kan Rehobowam*
*(1 Sarakuna 12.1-20)*

1 Rehobowam ya tafi Shekem, gama dukan Isra'ilawa sun je can don su naɗa shi
sarki. 2 Da Yerobowam ɗan Nebat ya ji wannan (a lokacin yana a Masar, inda ya
gudu daga Sarki Solomon ya tafi), sai ya dawo daga Masar. 3 Saboda haka suka aika a
zo da Yerobowam, sai shi da dukan Isra'ila suka je wurin Rehobowam suka ce masa.
4 "Mahaifinka ya sa mana kaya masu nauyi a kanmu, amma yanzu ka sauƙaƙa mana
aiki mai zafin nan da kuma kaya masu nauyin da ya sa a kanmu, mu kuwa za mu
bauta maka."

5 Rehobowam ya amsa, "Ku dawo gare ni cikin kwana uku." Saboda haka mutanen
suka watse.

6 Sai Sarki Rehobowam ya nemi shawarar dattawan da suka yi wa mahaifinsa
Solomon hidima a lokacin da yake da rai, ya tambaye suya ce, "Wace shawara za
ku ba ni don in amsa wa waɗannan mutane?"

7 Suka amsa suka ce, "In za ka ji tausayi waɗannan mutane ka kuma gamshe su,
ka kuma ba su amsar da ta dace, kullum za su zama bayinka."

8 Amma Rehobowam ya ƙi shawarar da dattawa suka ba shi ya kuma nemi
shawarar matasan da suka yi girma tare, suke kuma yin masa hidima. 9 Ya tambaye
su ya ce, "Mece ce shawararku? Yaya zan amsa wa waɗannan mutanen da suke ce
mini, 'Ka sauƙaƙa nauyin da mahaifinka ya sa a kanmu'?"

10 Matasan da suka yi girma tare shi suka amsa, "Faɗa wa mutanen da suke ce
maka, 'Mahaifinka ya sa kaya masu nauyi a kanmu, amma ka sauƙaƙa nauyinmu.'
Ka faɗa musu, 'Karamin yatsana ya fi ƙugun mahaifina kauri. 11 Mahaifina ya sa
muku kaya masu nauyi; zan ma sa mafi nauyi. Mahaifina ya bulale ku da bulala; zan
bulale ku da kunamai.' "

12 Bayan kwana uku sai Yerobowam da dukan mutane suka dawo wurin
Rehobowam, yadda sarki ya ce, "Ku dawo gare ni cikin kwana uku." 13 Sarki ya
amsa musu da kakkausar murya. Ya ƙi shawarar dattawan, 14 ya kuma bi shawarar
matasan ya ce, "Mahaifina ya sa muku kaya masu nauyi; zan ma sa mafi nauyi.
Mahaifina ya bulale ku da bulala; zan bulale ku da kunamai." 15 Saboda haka sarki bai
saurari mutane ba, gama wannan juyin al'amura daga Allah ne, don a cika maganar
UBANGIJI da ya yi ga Yerobowam ɗan Nebat ta wurin Ahiya mutumin Shilo.

16 Sa'ad da Isra'ila suka ga sarki ya ƙi yă saurare su, sai suka amsa wa sarki, suka
ce,

"Wanda rabo muke da shi a wurin Dawuda,
wanda sashe muke da shi daga ɗan Yesse?
Kowa yă koma tentinsa, ya Isra'ila!
Ka lura da gidanka, ya Dawuda!"

Saboda haka dukan Isra'ilawa suka tafi gida. 17 Amma game da Isra'ilawan da suke
zama a garuruwan Yahuda kuwa, Rehobowam ya ci gaba da yin mulki a bisansu.

18 Sarki Rehobowam ya aiki Hadoram wanda yake lura da aikin dole, amma
Isra'ilawa suka jajjefe shi da duwatsu har ya mutu. Sarki Rehobowam kuwa ya
gaggauta ya shiga keken yaƙinsa ya gudu zuwa Urushalima. 19 Ta haka Isra'ila ya
kasance cikin tawaye a kan gidan Dawuda har yă zuwa wannan rana.

# 11

*(1 Sarakuna 12.21-24)*

1 Sa'ad da Rehobowam ya iso Urushalima, ya tattara mayaƙa dubu ɗari takwas
daga gidan Yahuda da Benyamin, don su yi yaƙi da Isra'ila su sāke mai da mulki wa
Rehobowam.
2 Amma wannan maganar UBANGIJI ta zo ga Shemahiya mutumin Allah. 3 "Faɗa
wa Rehobowam ɗan Solomon sarkin Yahuda da kuma dukan Isra'ilawan da suke a
Yahuda da Benyamin, 4 'Ga abin da UBANGIJI ya ce kada ku haura don ku yi yaƙi
da 'yan'uwanku. Ku tafi gida kowannenku, gama wannan yi na ne.' " Saboda haka
suka yi biyayya ga maganar UBANGIJI suka kuma koma daga takawa don yaƙi da
Yerobowam.

*Rehobowam ya gina katanga kewaye da Yahuda*

5 Rehobowam ya zauna a Urushalima ya kuma gina garuruwa don kāriya a
cikin Yahuda. 6 Betlehem, Etam, Tekowa, 7 Bet-Zur, Soko, Adullam, 8 Gat, Maresha,
Zif, 9 Adorayim, Lakish, Azeka, 10 Zora, Aiyalon da Hebron. Waɗannan su ne
garuruwan katanga a cikin Yahuda da Benyamin. 11 Ya ƙarfafa kāriyarsu ya kuma sa
shugabannin mayaƙa a cikinsu, tare da tanadin abinci, man zaitun da kuma ruwan
inabi. 12 Ya sa garkuwoyi da māsu a cikin dukan biranen, ya kuma sa suka zama da
ƙarfi. Saboda haka Yahuda da Benyamin suka zama nasa.
13 Firistoci da Lawiyawa daga dukan yankuna ko'ina a Isra'ila suka haɗa kai da
shi. 14 Lawiyawa suka ma bar makiyayansu da mallakarsu, suka zo Yahuda da
Urushalima domin Yerobowam da 'ya'yansa maza sun ƙi su a matsayin firistocin
UBANGIJI. 15 Yerobowam ya naɗa firistocinsa domin masujadan kan tudu da kuma
domin gumakan nan na akuya da maraƙin da ya yi. 16 Waɗanda suke daga kowane
kabilar Isra'ila waɗanda suka sa zuciya a kan neman UBANGIJI, Allah na Isra'ila, suka
bi Lawiyawa zuwa Urushalima don su miƙa hadayu ga UBANGIJI Allah na kakanninsu.
17 Suka ƙarfafa mulkin Yahuda suka kuma goyi bayan Rehobowam ɗan Solomon
shekaru uku, suna tafiya a hanyoyin Dawuda da Solomon a wannan lokaci.

*Iyalin Rehobowam*

18 Rehobowam ya auri Mahalat, 'yar Yerimot ɗan Dawuda wadda Abihayil 'yar
Eliyab ɗan Yesse ta haifa. 19 Ta haifa masa 'ya'ya maza. Yewush, Shemariya da
Zaham. 20 Sa'an nan ya auri Ma'aka 'yar Absalom, wadda ta haifa masa Abiya, Attai,
Ziza da kuma Shelomit. 21 Rehobowam ya ƙaunaci Ma'aka 'yar Absalom fiye da
sauran matansa da ƙwarƙwaransa. Duka-duka dai ya auri mata goma sha takwas
da ƙwarƙwarai sittin, yana da 'ya'ya maza ashirin da takwas da 'ya'ya mata sittin.
22 Rehobowam ya naɗa Abiya ɗan Ma'aka yă zama babba yerima a cikin
'yan'uwansa, don dai yă naɗa shi sarki. 23 Ya yi hikima, ya watsar da waɗansu
'ya'yansa a dukan yankunan Yahuda da Benyamin, da kuma a dukan birane masu
katanga. Ya ba su tanadi mai yawa ya kuma aurar musu mata masu yawa.

# 12

*Shishak ya yaƙi Urushalima*
*(1 Sarakuna 14.25-28)*

1 Bayan mulkin Rehobowam ya kahu kamar sarki ya kuma yi ƙarfi, shi da dukan
Isra'ila suka yi biris da dokar UBANGIJI. 2 Domin sun yi rashin biyayya ga UBANGIJI,
saboda haka Shishak sarkin Masar ya yaƙi Urushalima a shekara ta biyar ta Sarki
Rehobowam. 3 Da kekunan yaƙi dubu ɗaya da ɗari biyu da kuma mahayan dawakai
dubu haɗe da mayaƙan Libiyawa, Sukkatawa da kuma Kushawa waɗanda suka wuce
ƙidaya suka zo tare da shi daga Masar, 4 ya ci biranen katanga na Yahuda har zuwa
Urushalima.

[5] Sai annabi Shemahiya ya zo wurin Rehobowam da kuma wajen shugabannin
Yahuda waɗanda suka taru a Urushalima don tsoron Shishak, ya kuma faɗa musu,
“Ga abin da UBANGIJI ya ce, ‘Kun yi biris da ni; saboda haka, yanzu na bashe ku ga
Shishak.’ ”
[6] Shugabannin Isra’ila da sarki suka ƙasƙantar da kansu suka ce, “UBANGIJI mai
adalci ne.”
[7] Sa’ad da UBANGIJI ya ga sun ƙasƙantar da kansu, sai wannan maganar UBANGIJI
ta zo wa Shemahiya, “Tun da yake sun ƙasƙantar da kansu, to, ba zan hallaka su ba,
amma zan cece su, ba zan kwararo fushina ta hannun Shishak a kan Urushalima ba.
[8] Duk da haka za su zama bayinsa, don su san bambanci tsakanin yin mini bauta da
kuma yin wa sarakunan sauran ƙasashe bauta.”
[9] Da Shishak sarkin Masar ya yaƙi Urushalima, sai ya kwashi ma’ajin haikalin
UBANGIJI da kuma ma’ajin fadan sarki. Ya kwashe kome da kome, har da garkuwoyin
zinariyar da Solomon ya yi. [10] Sai sarki Rehobowam ya ƙera garkuwoyin tagulla a
madadin na zinariya, ya sa su a hannun shugabannin matsara na mashigin gidan
sarki. [11] Duk sa’ad da sarki ya tafi haikalin UBANGIJI, masu tsaron sukan tafi tare da
shi, suna riƙe da garkuwoyi, daga baya kuma su mai da su a ɗakin tsaro.
[12] Gama Rehobowam ya ƙasƙantar da kansa, fushin UBANGIJI ya bar shi, ba a kuwa
hallaka shi ƙaƙaf ba. Tabbatacce an yi ’yan abubuwa masu kyau a Yahuda.

*(1 Sarakuna 14.21,29-31)*

[13] Sarki Rehobowam ya kafa kansa daram a Urushalima, ya kuma ci gaba a
matsayin sarki. Yana da shekara arba’in da ɗaya sa’ad da ya zama sarki, ya kuma yi
mulki shekara goma sha bakwai a Urushalima, birnin da UBANGIJI ya zaɓa daga dukan
kabilan Isra’ila wanda zai sa Sunansa. Sunan mahaifiyarsa Na’ama ce, ita mutuniyar
Ammon ce. [14] Ya aikata mugunta domin bai sa zuciyarsa ga neman UBANGIJI ba.
[15] Game da ayyukan mulkin Rehobowam, daga farko zuwa ƙarshe, ba a rubuce
suke a tarihin Shemahiya annabi da Iddo mai gani wanda yake zancen zuriyoyi ba?
Aka kasance da yaƙe-yaƙe tsakanin Rehobowam da Yerobowam. [16] Rehobowam ya
huta da kakanninsa aka kuma binne shi a Birnin Dawuda. Abiya ɗansa kuma ya gāje
shi a matsayin sarki.

# 13

*Abiya sarkin Yahuda*

*(1 Sarakuna 15.1-8)*

[1] A shekara ta sha takwas ta sarautar Yerobowam, Abiya ya zama sarkin Yahuda,
[2] ya kuma yi mulki a Urushalima shekaru uku. Sunan mahaifiyarsa Mikahiya ce, ’yar
Uriyel na Gibeya.

Aka kasance da yaƙe-yaƙe tsakanin Abiya da Yerobowam. [3] Abiya ya tafi yaƙi tare
da mayaƙa dubu ɗari huɗu jarumawa, Yerobowam kuwa ya ja dāgār yaƙi a kan
Abiya da mayaƙa dubu ɗari takwas jarumawa.
[4] Abiya ya tsaya a Dutsen Zemarayim, a ƙasar tudu ta Efraim ya ce, “Yerobowam
da dukan Isra’ila, ku saurare ni! [5] Ba ku san cewa UBANGIJI, Allah na Isra’ila ya ba da
sarautar Isra’ila ga Dawuda da zuriyarsa har abada ta wurin alkawarin gishiri ba?
[6] Duk da haka Yerobowam ɗan Nebat, ma’aikacin Solomon ɗan Dawuda, ya tayar wa
maigidansa, [7] sai ya tara wa kansa ’yan iska da mugayen mutane suka yi gāba da
Rehobowam ɗan Solomon. Rehobowam lokacin kuwa ba shi da wayo, don haka bai
iya tsai da su ba.
[8] “Yanzu kuna shirin yin tsayayya da mulkin UBANGIJI, wanda yake a hannuwan
zuriyar Dawuda. Tabbatacce ku ƙasaitacciyar mayaƙa ne kuma kuna tare da ku
maruƙan zinariyar da Yerobowam ya yi domin su zama allolinku. [9] Ba ku ne

kuka kori firistocin Ubangiji, ʼyaʼyan Haruna maza, da Lawiyawa kuka kuma zaɓi
firistocinku kamar yadda sauran alʼummai suke yi ba? Duk wanda ya zo ya miƙa
ɗan bijimi da raguna bakwai don yǎ tsarkake kansa, ya zama firist na gumaka ke
nan, ba na Allah ba.
10 "Gare mu kuwa, Ubangiji shi ne Allah, kuma ba mu yashe shi ba. Firistocin
da suke bauta wa Ubangiji ʼyaʼyan Haruna maza ne, Lawiyawa ne kuwa suke
taimakonsu. 11 Kowace safiya da kowace yamma sukan miƙa hadayun ƙonawa da
turare mai ƙanshi ga Ubangiji. Sukan shirya burodi a tsarkaken tebur mai tsabta,
sukan kuma ƙuna fitilu a alkukai kowace yamma. Muna kiyaye ƙaʼidodin Ubangiji
Allahnmu. Amma ku kun yashe shi. 12 Allah yana tare da mu; shi ne shugabanmu.
Firistocinsa tare da ƙahoni za su busa kirarin yaƙi a kanku. Mutanen Israʼila, kada
ku yi yaƙi da Ubangiji Allah na kakanninku, gama ba za ku yi nasara ba."
13 To, fa, Yerobowam ya aiki mayaƙa su zagaya daga baya, domin yayinda yake a
gaban Yahuda, sai ʼyan kwanto su kasance a bayansu. 14 Yahuda ya juya sai ya ga
cewa ana yaƙe su gaba da baya. Sai suka yi kuka ga Ubangiji. Firistoci suka busa
ƙahoni 15 mutanen Yahuda kuwa suka tā da kirarin yaƙi. Da ji kirarin yaƙi, Allah ya
fatattake Yerobowam da dukan Israʼila a gaban Abiya da Yahuda. 16 Israʼilawa suka
gudu a gaban Yahuda, Allah kuwa ya bashe su a hannuwansu. 17 Abiya da mutanensa
suka kashe su sosai, har mutum dubu ɗari biyar suka mutu a cikin jarumawan
Israʼila. 18 Aka cinye mutanen Israʼila a wannan lokaci, mutanen Yahuda kuwa suka
yi nasara domin sun dogara ga Ubangiji Allah na kakanninsu.
19 Abiya ya kori Yerobowam ya kuma ƙwace garuruwan Betel, Yeshana da Efron,
tare da ƙauyukan da suke kewaye daga gare shi. 20 Yerobowam bai sāke yin ƙarfi a
zamanin Abiya ba. Ubangiji ya buge shi ya kuma mutu.
21 Amma Abiya ya ƙara ƙarfi. Ya auri mata goma sha huɗu, ya kuma kasance da
ʼyaʼya maza ashirin da biyu da kuma ʼyaʼya mata goma sha shida.
22 Sauran ayyukan sauratar Abiya, abin da ya yi da abin da ya faɗa, a rubuce suke
a cikin rubuce-rubucen annabi Iddo.

# 14

1 Abiya kuwa ya huta tare da kakanninsa, aka kuma binne shi a Birnin Dawuda.
Asa ɗansa ya gāje shi a matsayin sarki, a zamaninsa kuma ƙasar ta zauna lafiya na
shekara goma.

### *Asa sarkin Yahuda*

2 Asa ya yi abin da yake da kyau da kuma daidai a gaban Ubangiji Allahnsa. 3 Ya
kawar da baƙin bagade da masujadai bisa tudu, ya farfashe keɓaɓɓun duwatsu, ya
kuma sassare ginshiƙan Ashera. 4 Ya umarci Yahuda su nemi Ubangiji Allah na
kakanninsu, su kuma yi biyayya da dokoki da kuma umarnansa. 5 Ya kawar da
masujadan kan tudu da bagadan turare a kowane gari a Yahuda, masarautar kuwa
ta zauna lafiya a ƙarƙashinsa. 6 Ya gina biranen katanga na Yahuda, da yake ƙasar
tana zaman lafiya. Babu wanda yake yaƙi da shi a waɗannan shekaru, gama Ubangiji
ya ba shi hutu.
7 Ya ce wa Yahuda, "Bari mu gina waɗannan garuruwa mu sa katanga kewaye da
su, da hasumiyoyi, ƙofofi da ƙyamare. Kasar har yanzu tamu ce domin mun nemi
Ubangiji Allahnmu, mun neme shi ya kuwa ba mu hutu a kowane gefe." Saboda haka
suka gina suka kuma yi nasara.
8 Asa ya kasance da mayaƙa dubu ɗari uku daga Yahuda, kintsatse da manyan
garkuwoyi da māsu, da kuma mayaƙa dubu ɗari biyu da dubu tamanin daga
Benyamin, riƙe da ƙananan garkuwoyi da kuma baka. Dukan waɗannan jarumawa
ne ƙwarai.

[9] Zera mutumin Kush ya taka ya fita don yă yaƙe su da babban runduna da kuma
kekunan yaƙi ɗari uku, ya kuma zo har Maresha. [10] Asa ya fita don yă ƙara da shi,
suka ja dāgā yaƙi a Kwarin Zefata kusa da Maresha.
[11] Sai Asa ya kira ga UBANGIJI Allahnsa ya ce, "UBANGIJI, babu wani kamar ka da zai
taimaki marar ƙarfi a kan mai ƙarfi. Ka taimake mu, ya UBANGIJI Allahnmu, gama
mun dogara a gare ka, kuma a cikin sunanka muka fito don mu yaƙi wannan babbar
runduna. Ya UBANGIJI, kai ne Allahnmu; kada ka bar mutum yă yi nasara a kanka."
[12] UBANGIJI fa ya bugi mutanen Kush a gaban Asa da Yahuda. Mutanen Kush suka
gudu, [13] Asa kuwa da mayaƙansa suka bi su har Gerar. Mutanen Kush suka mutu
a ranan nan har ba a iya ƙidaya, aka buge su a gaban UBANGIJI da rundunansa.
Mutanen Yahuda suka kwashi ganima sosai. [14] Suka hallaka dukan ƙauyukan kewaye
da Gerar, gama tsoron UBANGIJI ya kama su. Suka kwashi ganima na dukan ƙauyukan
nan, da yake akwai ganima sosai a can. [15] Suka kuma yaƙi sansanin makiyaya suka
kwashe tumaki da awaki da raƙuma. Suka koma Urushalima.

# 15

*Sauye-sauyen Asa*

[1] Sai Ruhun Allah ya sauko a kan Azariya ɗan Oded. [2] Ya fita ya je ya sadu da Asa ya
kuma faɗa masa, "Ka saurare ni, Asa da kuma dukan Yahuda da Benyamin. UBANGIJI
yana tare da ku sa'ad da kuke tare da shi. In kuka neme shi, za ku same shi, amma in
kuka yashe shi, zai yashe ku. [3] Tun da daɗewa Isra'ila ba su da Allah na gaskiya, babu
firist da zai koyar, kuma babu doka. [4] Amma cikin wahalarsu suka juya ga UBANGIJI,
Allah na Isra'ila, suka kuma neme shi, suka kuwa same shi. [5] A waɗancan kwanaki
akwai hatsari a yin tafiye-tafiye, gama dukan mazaunan ƙasashe suna cikin babbar
damuwa. [6] Wata ƙasa takan murƙushe wata, wani birni kuma yakan murƙushe
wani, domin Allah ya wahalshe su da kowace irin damuwa. [7] Amma game da ku, ku
ƙarfafa kada ku fid da zuciya, gama za a ba ku ladan aikinku."
[8] Sa'ad da Asa ya ji waɗannan kalmomin da annabcin Azariya ɗan Oded annabi
ya faɗa, sai ya sami ƙarfi hali. Ya kawar da gumaka masu banƙyama daga dukan
ƙasar Yahuda da Benyamin da kuma daga garuruwan da ya ci da yaƙi a ƙasar tudu ta
Efraim. Ya gyaggyara bagaden UBANGIJI da yake a gaban shirayin haikalin UBANGIJI.
[9] Sa'an nan ya tattara dukan Yahuda da Benyamin da kuma mutane daga Efraim,
Manasse da Simeyon waɗanda suke zaune a cikinsu, gama jama'a mai girma ta zo
wurinsa daga Isra'ila sa'ad da suka ga cewa UBANGIJI Allahnsa yana tare da shi.
[10] Suka taru a Urushalima a wata na uku na shekara ta goma sha biyar ta mulkin
Asa. [11] A lokacin suka miƙa hadaya bijimai ɗari bakwai da tumaki da kuma awaki
dubu bakwai ga UBANGIJI daga ganimar da suka dawo da ita. [12] Suka yi alkawari don
su nemi UBANGIJI Allah na kakanninsu, da dukan zuciyarsu da kuma dukan ransu.
[13] Aka kashe dukan waɗanda ba su nemi UBANGIJI, Allah na Isra'ila ba, ko ƙarami ko
babba, namiji ko ta mace. [14] Suka yi rantsuwa ga UBANGIJI da babbar murya, da ihu
da garayu da ƙahoni. [15] Dukan Yahuda suka yi farin ciki game da rantsuwar domin
sun yi rantsuwar gabagadi. Suka nemi Allah da gaske, suka kuma same shi. Saboda
haka UBANGIJI ya ba su hutu a kowane gefe.
[16] Sarki Asa ya tuɓe mahaifiyar mahaifiyarsa daga matsayinta na mahaifiyar
sarauniya, domin ta gina ginshiƙin banƙyama na Ashera. Asa ya rurrushe shi, ya
farfasa shi ya kuma ƙone shi a Kwarin Kidron. [17] Ko da yake bai kawar da masujadan
kan tudu daga Isra'ila ba, zuciyar Asa ta cika da bin UBANGIJI dukan kwanakinsa. [18] Ya
kawo azurfa da zinariya da kayayyaki a haikalin Allah waɗanda shi da mahaifinsa
suka keɓe.
[19] Ba a ƙara yin yaƙi ba sai a shekara ta talatin da biyar ta mulkin Asa.

# 16

*Shekarun ƙarshe na Asa*
*(1 Sarakuna 15.16-22)*
1 A shekara ta talatin da shida ta mulkin Asa, Ba'asha sarkin Isra'ila ya haura don
yǎ yaƙi Yahuda da Rama mai katanga, don kuma yǎ hana wani daga fita ko shiga
yankin Asa sarkin Yahuda.
2 Sai Asa ya ɗauki azurfa da zinariya daga ma'ajin haikalin UBANGIJI da kuma na
fadansa ya aika wa Ben-Hadad sarkin Aram, wanda yake mulki a Damaskus. 3 Ya
ce, "Bari yarjejjeniya ta kasance tsakani na da kai kamar yadda ya kasance tsakanin
mahaifina da mahaifinka. Dubi ina aika maka azurfa da zinariya. Yanzu ka yanke
yarjejjeniya da Ba'asha sarkin Isra'ila domin yǎ janye daga gare ni."
4 Ben-Hadad ya yarda da Sarki Asa ya kuma aika da manyan hafsoshin mayaƙansa
a kan garuruwan Isra'ila. Suka ci Iyon, Dan, Abel-Mayim[*] da kuma dukan biranen
ajiya na Naftali. 5 Da Ba'asha ya ji wannan, ya daina ginin Rama ya yashe aikinsa.
6 Sa'an nan Sarki Asa ya kawo dukan mutanen Yahuda, suka kuma kwashe duwatsu
da katako daga Rama waɗanda Ba'asha yake amfani da su. Da su ne Asa ya gina
Geba da Mizfa.
7 A lokacin Hanani mai duba ya zo wurin Asa sarkin Yahuda ya ce masa, "Don ka
dogara ga sarkin Aram, ba kuwa ga UBANGIJI Allahnka ba ne mayaƙan sarkin Aram
sun kuɓuce daga hannunka. 8 Ai, Kushawa da Libiyawa rundunar sojoji ne masu
yawan gaske, suna kuma da kekunan yaƙi da mahayan dawakai masu yawa ƙwarai.
Amma duk da haka, saboda ka dogara ga UBANGIJI, ya kuwa ba da su cikin hannunka.
9 Gama gaban UBANGIJI yana ko'ina a duniya don yǎ ƙarfafa waɗanda zukatansu suke
binsa cikin aminci. Ka yi wauta, daga yanzu nan gaba za ka yi ta yaƙi."
10 Sai Asa ya yi fushi sosai da mai duban saboda wannan; ya yi fushi ƙwarai har ya
sa aka jefa shi a kurkuku. A lokaci guda kuma Asa ya fara gwada wa mutane azaba.
*(1 Sarakuna 15.23,24)*
11 Ayyukan mulkin Asa, daga farko zuwa ƙarshe, suna a rubuce a littafin sarakunan
Yahuda da Isra'ila. 12 A shekara ta talatin da tara ta mulkinsa, Asa ya kamu da wata
cuta a ƙafarsa. Ko da yake cutar ta yi tsanani, duk d haka ma a cikin ciwonsa bai
nemi taimako daga UBANGIJI ba, sai dai daga likitoci. 13 Sa'an nan a shekara ta arba'in
da ɗaya ta mulkinsa, Asa ya mutu ya kuma huta tare da kakanninsa. 14 Suka binne
shi a kabarin da ya fafe wa kansa a Birnin Dawuda. Suka sa shi a makara wadda
aka rufe da kayan yaji da kuma turare dabam-dabam da aka niƙa, suka kuma ƙuna
babbar wuta don girmama shi.

# 17

*Yehoshafat sarkin Yahuda*
1 Yehoshafat ɗansa ya gāje shi a matsayin sarki ya kuma kahu sosai gāba da Isra'ila.
2 Ya kafa mayaƙa a dukan biranen katangar Yahuda, ya kuma sa runduna a Yahuda
da kuma a garuruwan Efraim da mahaifinsa Asa ya ci da yaƙi.
3 UBANGIJI kuwa yana tare da Yehoshafat domin a shekarunsa na farko-farko ya yi
tafiya a hanyoyin da kakansa Dawuda ya bi. Bai nemi shawarar Ba'al ba 4 amma ya
nemi Allah na kakansa ya kuma bi umarnansa a maimakon ayyukan da Isra'ila ke yi.
5 UBANGIJI ya kafa mulkin a ƙarƙashin ikonsa; dukan Yahuda kuwa suka kawo kyautai
wa Yehoshafat, ta haka ya yi arziki sosai da kuma girma. 6 Zuciyarsa ta duƙufa ga
hanyoyin UBANGIJI, bugu da ƙari, ya kawar masujadan kan tudu da ginshiƙan Ashera
daga Yahuda.

[*] **16:4** An kuma san shi da Abel-Bet-Ma'aka

7 A shekara ta uku ta mulkinsa, ya aiki ma'aikatansa Ben-Hayil, Obadiya, Zakariya,
Netanel da Mikahiya su yi koyarwa a gararuwan Yahuda. 8 Tare da su akwai waɗansu
Lawiyawa, Shemahiya, Netaniya, Zebadiya, Asahel, Shemiramot, Yehonatan, Adoniya,
Tobiya da Tob Adoniya, da kuma firistoci Elishama da Yehoram. 9 Suka yi koyarwa a
dukan Yahuda, suna ɗauke da Littafin Dokar UBANGIJI tare da su; suka tafi ko'ina a
dukan gararuwan Yahuda suka koyar da mutane.
10 Tsoron UBANGIJI ya kama dukan masarautun ƙasashen da suke kewaye da
Yahuda, har ba su yi yaƙi da Yehoshafat ba. 11 Waɗansu Filistiyawa suka kawo wa
Yehoshafat kyautai da azurfa a matsayin haraji, Larabawa kuwa suka kawo masa
garkuna, raguna dubu bakwai da ɗari bakwai da kuma awaki dubu bakwai da ɗari
bakwai.
12 Yehoshafat ya yi ta ƙaruwa a ƙarfi; ya gina katanga da biranen ajiya a Yahuda
13 da kuma tanade-tanade masu yawa a gararuwan Yahuda. Ya kuma ajiye gogaggu
mayaƙa a Urushalima. 14 Ɗaukar da aka yi musu bisa ga iyalai yana kamar haka.

Daga Yahuda, shugaban ƙungiya 1,000.
Adna ne shugaba, tare da jarumawa 300,000;
15 biye da shi, Yehohanan shi ne shugaba, yana da sojoji 280,000;
16 biye da shi, Amasiya ɗan Zikri, wanda ya ba da kansa da yardar rai don hidimar
UBANGIJI, yana da sojoji 200,000.
17 Daga Benyamin,
Eliyada, jarumi soja, yana da sojoji 200,000 riƙe da baka da garkuwoyi;
18 biye da shi, Yehozabad, yana da sojoji 18,000 shiryayyu don yaƙi.

19 Waɗannan su ne suka yi wa sarki hidima, ban da waɗanda aka sa a biranen
katanga ko'ina a Yahuda.

# 18

*Mikahiya ya yi annabci a kan Ahab*
*(1 Sarakuna 22.1-28)*

1 Yanzu fa Yehoshafat ya wadace ƙwarai yana kuma da girma, ya kuma haɗa kansa
da Ahab ta wurin aure. 2 Bayan 'yan shekaru sai ya gangara don yă ziyarci Ahab a
Samariya. Ahab kuwa ya yanka tumaki da shanu masu yawa dominsa da kuma
mutanen da suke tare da shi, ya kuma lallashe shi yă yaƙi Ramot Gileyad. 3 Ahab
sarkin Isra'ila ya tambayi Yehoshafat sarkin Yahuda ya ce, "Za ka tafi tare da ni mu
yaƙi Ramot Gileyad?"
Yehoshafat ya amsa ya ce, "Ni kamar kai ne, kuma mutanena kamar naka ne; za
mu tafi tare da kai a yaƙin." 4 Amma Yehoshafat ya kuma ce wa sarkin Isra'ila, "Da
fari mu nemi bishewar UBANGIJI."
5 Saboda haka sarkin Isra'ila ya tattara annabawa duka, mutane ɗari huɗu, ya
kuma tambaye su, "Mu tafi yaƙi a kan Ramot Gileyad ko kada mu tafi?"
Suka amsa "Tafi, gama Allah zai ba da shi cikin hannun sarki."
6 Amma Yehoshafat ya yi tambaya ya ce, "Babu wani annabin UBANGIJI a nan da za
mu tambaya?"
7 Sarki Isra'ila ya amsa wa Yehoshafat, "Akwai guda har yanzu mai suna Mikahiya
ɗan Imla, za mu iya nemi nufin UBANGIJI daga gare shi, sai dai ba na sonsa domin
bai taɓa yin annabci wani abu mai kyau game da ni ba, sai kullum masifa."
Yehoshafat ya amsa ya ce, "Kada sarki yă faɗa haka."
8 Saboda haka sarkin Isra'ila ya kira ɗaya daga cikin ma'aikatansa ya ce, "A kawo
Mikahiya ɗan Imla nan da nan."

9 Saye da rigunan sarakuna, sarki Isra'ila da Yehoshafat sarkin Yahuda suna zaune
a kan kujerunsu na mulki a masussuka ta ƙofar shigar Samariya, tare da dukan
annabawa suna ta annabci a gabansu. 10 To, fa, Zedekiya ɗan Kena'ana ya yi ƙahonin
ƙarfe, ya kuma furta, "Ga abin da UBANGIJI ya ce, 'Da waɗannan za ka sassoki
Arameyawa sai sun hallaka.' "

11 Dukan sauran annabawan suka yi irin annabcin nan. Suka ce, "A haura zuwa
Ramot Gileyad a yi nasara, gama UBANGIJI zai ba da shi cikin hannun sarki."

12 Ɗan saƙon da ya tafi don yă kawo Mikahiya kuwa ya ce masa, "Duba, kowannen
a cikin annabawa ya yi faɗin nasara wa sarki. Don haka kai ma ka yi maganar da za
tă gamshi sarki kamar yadda suka yi."

13 Amma Mikahiya ya ce, "Na rantse da ran UBANGIJI, zan faɗa masa kawai abin da
Allahna ya faɗa."

14 Da suka iso, sarki ya tambaye shi, "Mika, mu tafi mu yaƙi Ramot Gileyad, ko kada
mu tafi?"

Ya amsa, "Kai masa yaƙi za ka kuwa yi nasara, gama za a ba da su a hannunka."

15 Sarki ya ce masa, "Sau nawa zan sa ka rantse don ka faɗa gaskiya a cikin sunan
UBANGIJI?"

16 Sa'an nan Mikahiya ya amsa, "Na ga dukan Isra'ila sun warwatsu a kan tuddai
kamar tumakin da ba su da makiyaya, kuma UBANGIJI ya ce, 'Waɗannan mutane ba
su da maigida. Bari kowanne yă tafi gida cikin salama.' "

17 Sarkin Isra'ila ya ce wa Yehoshafat, "Ban faɗa maka cewa bai taɓa yin annabci
wani abu mai kyau game da ni, in ba masifa ba?"

18 Mikahiya ya ci gaba, "Saboda haka sai ka ji maganar UBANGIJI. Na ga UBANGIJI
yana zama a kan kursiyinsa tare da dukan rundunar sama tsaye a damansa da
hagunsa. 19 UBANGIJI kuwa ya ce, 'Wa zai ruɗe Ahab sarki Isra'ila zuwa yaƙi da
Ramot Gileyad da kuma zuwa mutuwarsa a can?'

"Wani ya ba da wata shawara, wani kuma wata dabam. 20 A ƙarshe, wani ruhu ya
zo gaba, ya tsaya a gaban UBANGIJI ya ce, 'Zan ruɗe shi.'

"UBANGIJI ya yi tambaya, 'Ta wace hanya?'

21 "Ya ce, 'Zan tafi in zama ruhun ƙarya a bakunan dukan annabawansa.'

"UBANGIJI ya ce, 'Za ka yi nasara a ruɗinsa. Ka tafi, ka yi haka.'

22 "To yanzu, UBANGIJI ya sa ruhun ruɗu a bakunan waɗannan annabawanka.
UBANGIJI ya ƙayyade masifa dominka."

23 Sai Zedekiya ɗan Kena'ana ya haura ya mari Mikahiya a fuska. Ya ce, "Ta wace
hanya ce ruhun UBANGIJI ya fita daga gare ni ya zo ya yi magana da kai?"

24 Mikahiya ya amsa ya ce, "Za ka gane a ranar da ka je ka ɓuya a can cikin ɗaki."

25 Sa'an nan sarkin Isra'ila ya umarta, "Dauki Mikahiya ku aika da shi zuwa ga
Amon mai mulkin birni da kuma ga Yowash ɗan sarki, 26 ku ce ga abin da sarki ya
ce, 'Ku jefa wannan mutum a kurkuku kada kuma ku ba shi wani abu sai dai burodi
da ruwa har sai na dawo lafiya.' "

27 Mikahiya ya furta ya ce, "Idan har ka dawo lafiya, to, UBANGIJI bai yi magana ta
wurina ba." Ya kuma ƙara da cewa, "Dukanku mutane, ku lura da maganata!"

### *An kashe Ahab a Ramot Gileyad*
### *(1 Sarakuna 22.29-35)*

28 Saboda haka sarkin Isra'ila da Yehoshafat sarkin Yahuda suka haura zuwa Ramot
Gileyad. 29 Sarkin Isra'ila ya ce wa Yehoshafat, "Zan ɓad da kama in shiga yaƙin,
amma ka sa kayanka na sarauta." Saboda haka sarkin Isra'ila ya ɓad da kama ya
shiga cikin yaƙin.

30 To, fa, sarkin Aram ya umarce shugabannin keken yaƙinsa ya ce, "Kada ku yaƙi
kowa, ƙarami ko babba, sai dai sarkin Isra'ila." 31 Sa'ad da shugabannin kekunan

yaƙi suka ga Yehoshafat, sai suka yi tsammani, “Wannan ne sarkin Isra’ila.” Saboda haka suka juya don su yaƙe shi, amma Yehoshafat ya yi ihu, UBANGIJI kuma ya taimake shi. Allah ya janye su daga gare shi,
32 gama sa’ad da shugabannin keken yaƙi suka ga cewa ba shi ne sarkin Isra’ila ba, sai suka daina binsa.
33 Amma wani ya harba kibiya haka kawai, sai kibiyar ta sami sarki Ahab na Isra’ila a kafaɗa tsakanin rigar yaƙinsa na ƙarfe da ƙarfen ƙirjinsa. Sai sarki ya ce wa mai tuƙan keken yaƙi, “Juya ka fitar da ni daga wurin yaƙin. An ji mini rauni.”
34 Duk yini yaƙi ya yi ta cin gaba, sarkin Isra’ila kuwa ya jingina kansa a cikin keken yaƙinsa yana duban Arameyawa har yamma. Sa’an nan a fāɗuwar rana sai ya mutu.

# 19

1 Sa’ad da Yehoshafat sarkin Yahuda ya dawo zuwa fadansa a Urushalima lafiya,
2 Yehu mai duba, ɗan Hanani, ya fita don yă tarye shi, ya kuma ce wa sarki, “Ya yi kyau ke nan da ka taimaki mugu ka kuma ƙaunaci* waɗanda suke ƙin UBANGIJI? Da yake ka yi haka fushin UBANGIJI yana a kanka
3 Duk da haka an sami wani abin kirki a wurinka, gama ka kawar da ginshiƙan Ashera a ƙasar, ka kuma sa zuciyarka a kan neman Allah.”

*Yehoshafat ya naɗa alƙalai*

4 Yehoshafat ya zauna a Urushalima, ya kuma fita yana shiga cikin mutane daga Beyersheba zuwa ƙasar tudun Efraim ya kuma juyar da su ga UBANGIJI Allah na kakanninsu.
5 Ya naɗa alƙalai a kowanne daga cikin biranen katanga na Yahuda a ƙasar.
6 Ya faɗa musu, “Ku lura da abin da kuke yi, gama shari’ar da kuke yi ba ta mutum ba ce, amma ta UBANGIJI ce, yana tare da ku sa’ad da kuke yanke shari’a.
7 Yanzu fa ku ji tsoron UBANGIJI. Ku yi hankali a kan abin da kuke yi, gama UBANGIJI Allahnmu ba ya sonkai ko nuna wariya ko cin hanci.”
8 A Urushalima kuma, Yehoshafat ya naɗa waɗansu Lawiyawa, firistoci da kawunan iyalan Isra’ilawa don su tabbatar da an bi dokar UBANGIJI, su kuma sasanta tsakanin mutane. A Urushalima za su zauna.
9 Ya ba su waɗannan umarnai, “Ku yi aikinku da aminci da tsoron UBANGIJI da dukan zuciyarku.
10 Cikin kowane batun da ya zo gabanku daga ’yan’uwanku waɗanda suke zama a birane, ko batun na kisa ne ko kuwa waɗansu batuttuwan da suka shafi doka, umarnai, ƙa’idodi ko farillai, dole ku ja musu kunne kada su yi wa UBANGIJI zunubi; in ba haka ba fushinsa zai sauko a kanku da ’yan’uwanku. Ku yi wannan, ta haka ba za ku kuwa yi zunubi ba.
11 “Amariya, babban firist, shi ne zai shugabance ku a kan dukan al’amuran da suke na wajen UBANGIJI, Zebadiya ɗan Ishmayel kuwa, shugabanku a kan dukan al’amuran da suka shafi sarki, Lawiyawa kuma za su zama a matsayin manya a gabanku. Ku yi abubuwa da ƙarfin hali, bari kuma UBANGIJI yă kasance tare da masu yin gaskiya.”

# 20

*Yehoshafat ya ci Mowab da Ammon a yaƙi*

1 Bayan wannan, Mowabawa da Ammonawa tare da waɗansu Meyunawa suka zo su yaƙi Yehoshafat.
2 Sai waɗansu mutane suka zo suka faɗa wa Yehoshafat, “Ga babban runduna tana zuwa a kanka daga Edom, daga ƙetaren Teku, daga Aram. Ta ma kai Hazazon Tamar” (wato, En Gedi).
3 A firgice, Yehoshafat ya yanke shawara yă nemi nufin UBANGIJI, ya kuma yi shelar azumi a dukan Yahuda.
4 Mutanen Yahuda suka taru gaba ɗaya don su nemi taimako daga wurin UBANGIJI, tabbatacce suka fito daga kowane garin Yahuda don su neme shi.

* **19:2** Ko kuwa ka haɗa kai da

5 Sa'an nan Yehoshafat ya miƙe tsaye a taron Yahuda da Urushalima a haikalin
UBANGIJI a sabon filin 6 ya ce,
"Ya UBANGIJI Allah na kakanninmu, ba kai ne Allah wanda yake sama ba? Kana
mulki a bisa dukan mulkokin ƙasashe. Iko da girma suna a hannunka, kuma ba
wanda zai iya tsayayya da kai. 7 Ya Allahnmu, ba kai ba ne ka kore mazaunan
wannan ƙasa a gaban mutanenka Isra'ila ka kuma ba da ita har abada ga zuriyar
Ibrahim abokinka? 8 Sun yi zama a cikinta suka kuma yi gina wuri mai tsarki
a cikinta domin Sunanka cewa, 9 'In masifa ta zo mana, ko takobin hukunci, ko
annoba ko yunwa, za mu tsaya a gabanka a gaban wannan haikalin da yake ɗauke
da Sunanka, mu kuma yi kuka gare ka cikin azaba, za ka kuwa ji mu, ka cece mu.'
10 "Yanzu kuma ga mutanen Ammon, da na Mowab, da na Dutsen Seyir, waɗanda
ka hana Isra'ilawa su kai musu yaƙi sa'ad da suka fito daga ƙasar Masar, su ne
mutanen da Isra'ila suka ƙyale, ba su hallaka su ba. 11 Yau ga yadda suke so su
biya mu. Su suke so su kore mu daga ƙasar da ka ba mu gādo. 12 Ya Allahnmu, ba
za ka hukunta su ba? Gama ba mu da ƙarfin fuskantar wannan babbar rundunar
da take so ta yaƙe mu. Ba mu san abin da za mu yi ba, mu dai mun zuba maka
ido."
13 Dukan mazan Yahuda, tare da matansu da yaransu da ƙananansu, suka tsaya a
gaban UBANGIJI.
14 Sa'an nan Ruhun UBANGIJI ya sauko a kan Yahaziyel ɗan Zakariya, ɗan Benahiya,
ɗan Yehiyel, ɗan Mattaniya, wani Balawe kuma zuriyar Asaf, yayinda yake tsaye a
cikin taron.
15 Ya ce, "Saurara, Sarki Yehoshafat da dukan waɗanda suke zama a Yahuda da
Urushalima! Ga abin da UBANGIJI ya ce muku, 'Kada ku ji tsoro ko ku fid da zuciya
saboda wannan babbar runduna. Gama yaƙin ba naku ba ne, amma na Allah. 16 Gobe
ku fito ku gangara ku yaƙe su. Za su yi ta haurawa ta Mashigin Ziz, ku kuwa za ku
same su a ƙarshen kwari a Hamadan Yeruwel. 17 Ba lalle ba ne ku yi wannan yaƙi.
Ku dai, ku ja dāgā, ku tsaya kurum ku ga nasarar da UBANGIJI zai ba ku, ya Yahuda
da Urushalima. Kada ku ji tsoro; kada ku karai. Ku fito don ku fuskance su gobe,
UBANGIJI kuwa zai kasance tare ku.' "
18 Yehoshafat ya rusuna da fuskarsa har ƙasa, dukan mutanen Yahuda da
Urushalima suka fāɗi rubda ciki suka yi sujada a gaban UBANGIJI. 19 Sa'an nan
waɗansu Lawiyawa daga Kohatawa da Korayawa suka tashi tsaye suka yabe UBANGIJI,
Allah na Isra'ila, da babbar murya sosai.
20 Da sassafe suka tashi suka nufi Hamadan Tekowa. Yayinda suka kama hanya,
Yehoshafat ya tsaya ya ce, "Ku saurare ni, Yahuda da mutanen Urushalima! Ku
amince da UBANGIJI Allahnku za a kuwa kafa ku; ku amince da annabawansa za ku
kuwa yi nasara." 21 Bayan suka yi shawara tare da shugabanni, sai ya zaɓi mutanen
da za su ja gaban sojoji suna waƙa ga UBANGIJI suna yabonsa saboda tsarkinsa suna
cewa,
"Ku yi godiya ga UBANGIJI,
gama ƙaunarsa dawwammamiya ce har abada."
22 Da suka fara waƙa, suna kuma yabo, sai UBANGIJI ya kai hari a kan mutanen
Ammon da Mowab da Dutsen Seyir, waɗanda suka kawo hari a Yahuda, aka kuwa
ci su da yaƙi. 23 Mutanen Ammon da Mowab suka tasar wa mazaunan Dutsen Seyir,
suka hallaka su ƙaƙaf. Sa'ad da suka karkashe mazaunan Seyir sai suka fāɗa wa
juna, suka yi ta hallaka juna.
24 Sa'ad da mutanen Yahuda suka zo wurin da yake fuskantar hamada, suka duba
ta wajen babban rundunar, sai suka ga gawawwaki birjik a ƙasa; babu wani wanda
ya kuɓuta. 25 Sa'ad da Yehoshafat da jama'arsa suka je kwasar ganima, sai suka
sami shanu masu yawan gaske, da kayayyaki, da tufafi, da abubuwa masu daraja,

waɗanda suka yi ta kwasa har suka gaji. Kwana uku suka yi suna kwasar ganimar
saboda yawanta. [26] A rana ta huɗu sai suka taru a Kwarin Beraka, inda suka yabi
UBANGIJI. Wannan ne ya sa ake kiransa Kwarin Beraka* har wa yau.
[27] Sa'an nan Yehoshafat ya jagoranci dukan mutanen Yahuda da Urushalima suka
dawo da farin ciki zuwa Urushalima, gama UBANGIJI ya ba su dalilin farin ciki a kan
abokan gābansu. [28] Suka shiga Urushalima suka shiga haikalin UBANGIJI da kiɗin
molaye da sarewa da kuma garayu.
[29] Tsoron Allah ya kama dukan mulkokin ƙasashe sa'ad da suka ji yadda UBANGIJI
ya yi yaƙi a kan abokan gāban Isra'ila. [30] Mulkin Yehoshafat kuwa ya zauna lafiya,
gama Allahnsa ya ba shi hutu a kowane gefe.

### *Karshen mulkin Yehoshafat*
*(1 Sarakuna 22.41-50)*

[31] Ta haka Yehoshafat ya yi mulki a bisa Yahuda. Yana da shekara talatin da biyar
sa'ad da ya zama sarkin Yahuda, ya kuma yi mulki a Urushalima shekara ashirin da
biyar. Sunan mahaifiyarsa Azuba ce, 'yar Shilhi. [32] Ya yi tafiya a hanyoyin mahaifinsa
Asa bai kuwa kauce daga gare su ba; ya yi abin da yake daidai a gaban UBANGIJI.
[33] Duk da haka ba a kawar da masujadai kan tudu ba, domin har yanzu mutanen ba
su tsayar da zukatansu ga Allahn kakanninsu ba.
[34] Sauran ayyukan mulkin Yehoshafat, daga farko zuwa ƙarshe, an rubuta su a
tarihin Yehu ɗan Hanani, waɗanda aka rubuta a littafin sarakunan Isra'ila.
[35] Daga baya, Yehoshafat sarkin Yahuda ya haɗa kai da Ahaziya sarkin Isra'ila,
wanda yake da laifin mugunta. [36] Ya yarda da shi su gina jiragen ruwan kasuwanci.
Bayan aka gina waɗannan a Eziyon Geber, [37] Eliyezer ɗan Dodabahu na Maresha
ya yi annabci a kan Yehoshafat cewa, "Domin ka haɗa kai da Ahaziya, UBANGIJI zai
hallaka abin da ka yi." Jiragen ruwan kuwa suka farfashe, ba a kuwa iya sa su je
kasuwanci ba.

## 21

[1] Yehoshafat ya huta tare da kakanninsa, aka kuma binne shi tare da su a Birnin
Dawuda. Sai Yehoram ɗansa ya gāje shi a matsayin sarki.
*(2 Sarakuna 8.16-24)*
[2] 'Yan'uwan Yehoram, 'ya'yan Yehoshafat maza su ne, Azariya, Yehiyel, Zakariya,
Azariyahu, Mika'ilu da Shefatiya. Dukan waɗannan su ne 'ya'yan Yehoshafat sarkin
Isra'ila* maza. [3] Mahaifinsu ya ba su kyautai masu yawa na azurfa da zinariya da
kayayyaki masu daraja, tare da birane masu katanga a Yahuda, amma ya ba da mulki
ga Yehoram domin shi ne ɗan farinsa.

### *Yehoram sarkin Yahuda*

[4] Sa'ad da Yehoram ya kafa kansa sosai a bisa mulkin mahaifinsa, sai ya kashe
dukan 'yan'uwansa da takobi tare da waɗansu sarakunan Isra'ila. [5] Yehoram yana
da shekara talatin da biyu sa'ad da ya zama sarki, ya kuma yi mulki a Urushalima
shekara takwas. [6] Ya yi tafiya a hanyoyin sarakunan Isra'ila, kamar yadda gidan Ahab
ta yi, gama ya auri 'yar Ahab. Ya aikata mugayen ayyuka a idon UBANGIJI. [7] Duk da
haka, domin alkawarin da UBANGIJI ya yi wa Dawuda, UBANGIJI bai so yǎ hallaka
gidan Dawuda ba. UBANGIJI ya riga ya yi alkawari zai ci gaba da riƙe fitila domin
Dawuda da zuriyarsa har abada.
[8] A zamanin Yehoram, Edom ya tayar wa Yahuda ya kuma naɗa sarkinsa. [9] Saboda
haka Yehoram ya tafi can tare da shugabannin sojojinsa da kuma dukan keken

* **20:26** Beraka yana nufin yabo. * **21:2** Wato, Yahuda, kamar yadda yake sau da sau a 2 Tarihi.

yaƙinsa. Mutanen Edom suka kewaye shi da shugabannin keken yaƙinsa, amma
ya tashi ya fatattaki su da dare. 10 Har yă zuwa yau Edom na tawaye a kan Yahuda.
Libna ya yi tawaye a lokaci guda, domin Yehoram ya yashe UBANGIJI Allah na
kakanninsa. 11 Ya gina masujadan kan tudu a tuddan Yahuda, ya kuma sa mutanen
Urushalima suka yi karuwanci, ya sa Yahuda suka kauce.
12 Yehoram ya sami wasiƙa daga Iliya annabi, wadda ta ce,

“Ga abin da UBANGIJI Allah na kakanka Dawuda ya ce, ‘Ba ka yi tafiya a hanyoyin
mahaifinka Yehoshafat ko Asa sarkin Yahuda ba. 13 Amma ka yi tafiya a hanyoyin
sarakunan Isra’ila, ka sa Yahuda ya kauce, ka kuma sa mutanen Urushalima suka yi
karuwanci, kamar yadda gidan Ahab ta yi. Ka kuma kashe ’yan’uwanka, membobi
gidan mahaifinka, mutanen da suka fi ka kirki. 14 Saboda haka a yanzu UBANGIJI
yana shirin ya bugi mutanenka, ’ya’yanka maza, matanka da kuma kome da yake
naka, da bugu mai ƙarfi. 15 Kai kuma za ka kamu da ciwon hanji wanda zai yi ta
cinka kowace rana sai har hanjinka sun fito.’ ”

16 UBANGIJI ya sa Filistiyawa da Larabawa waɗanda suke zama kusa da Kushawa
su yi gāba da Yehoram 17 Suka yaƙi Yahuda, suka kai masa hari, suka kwashe dukan
abubuwa masu kyau da suka samu a fadan sarki, tare da ’ya’yansa maza da kuma
matansa. Ba wanda aka bari, sai dai Ahaziya autansa.
18 Bayan dukan wannan, sai UBANGIJI ya sa wa Yehoram cuta marar warkarwa ta
ciki. 19 Cikin lokaci, a ƙarshen shekara ta biyu, sai hanjin cikinsa suka fito saboda
cutar, ya kuma mutu cikin tsananin zafi. Mutanensa suka hura wuta don girmama
shi, kamar yadda suka yi wa kakanninsa.
20 Yehoram yana da shekara talatin da biyu sa’ad da ya zama sarki, ya kuma yi
mulki a Urushalima shekara takwas. Ya mutu, ba ma wanda ya kula, aka kuma
binne shi a Birnin Dawuda, amma ba a makabartan sarakuna ba.

# 22

*Ahaziya sarkin Yahuda*
*(2 Sarakuna 8.25-29; 9.21,27,28)*

1 Mutanen Urushalima suka mai da Ahaziya, autan Yehoram, sarki a madadinsa, da
yake ’yan hari, waɗanda suka zo tare da Larabawa cikin sansani, sun kashe dukan
manyan ’ya’yansa. Saboda haka Ahaziya ɗan Yeroham sarkin Yahuda ya fara mulki.
2 Ahaziya yana da shekara ashirin da biyu sa’ad da ya zama sarki, ya kuma yi mulki
a Urushalima shekara guda. Sunan mahaifiyarsa Ataliya ce, jikanyar Omri.
3 Shi ma ya yi tafiya a hanyoyin gidan Ahab, gama mahaifiyarsa ta ƙarfafa shi yă yi
abin da ba shi da kyau. 4 Ya aikata mugayen ayyuka a gaban UBANGIJI, yadda gidan
Ahab ta yi, gama bayan mutuwar mahaifinsa, sai gidan Ahab ta zama masu ba shi
shawara, shawarar da ta kai shi ga lalacewa. 5 Ya kuma bi shawararsu sa’ad da ya
tafi tare da Yoram ɗan Ahab sarkin Isra’ila don yă yaƙi Hazayel sarkin Aram a Ramot
Gileyad. Sai Arameyawa suka yi wa Yoram rauni; 6 saboda haka ya dawo Yezireyel
don yă yi jinyar raunin da suka yi masa a Rama cikin yaƙinsa da Hazayel sarkin
Aram.
Sa’an nan Azariya ɗan Yehoram sarkin Yahuda ya gangara zuwa Yezireyel don yă
ga Yoram ɗan Ahab domin ya ji rauni.
7 Ta wurin ziyarar Yoram, Allah ya kawo fāɗuwar Ahaziya. Sa’ad da Ahaziya ya
iso, ya tafi tare da Yoram domin yă sadu da Yehu ɗan Nimshi, wanda UBANGIJI ya
shafe don yă hallaka gidan Ahab. 8 Yayinda Yehu yake hukunta wa gidan Ahab, sai
ya sami fadawan Yahuda da kuma ’ya’yan dangin Ahaziya maza, waɗanda suke yi wa
Ahaziya hidima, sai ya kashe su. 9 Ya kuma sa aka nemi Ahaziya. Aka kamo shi sa’ad
da ya ɓuya a Samariya, suka kawo shi wurin Yehu, suka kashe shi, suka binne shi,

gama sun ce, “Shi jikan Yehoshafat ne, wanda ya nemi UBANGIJI da dukan zuciyarsa.” Ta haka babu wani a gidan Ahaziya da yake da ƙarfin cin gaba da mulkin.

*Ataliya da Yowash*
*(2 Sarakuna 11.1-3)*

10 Sa’ad da Ataliya mahaifiyar Ahaziya ta ga cewa ɗanta ya mutu, sai ta tashi ta
hallaka dukan ’yan gidan sarautar Yahuda. 11 Amma Yehosheba, ’yar Sarki Yehoram,
ta ɗauki Yowash ɗan Ahaziya ta sace shi daga cikin ’ya’yan gidan sarauta waɗanda
ake shiri a kashe, ta sa shi tare da mai renonsa a ɗakin kwana. Haka fa, Yehosheba
’yar sarki Yoram, matar Yehohiyada firist, ta yi, gama ita ’yar’uwar Ahaziya ce, ta
ɓoye Yowash don kada Ataliya tă kashe shi. 12 Ya kasance a ɓoye tare da su a haikalin
Allah shekara shida, yayinda Ataliya take mulkin ƙasar.

# 23

*(2 Sarakuna 11.4-21)*

1 A shekara ta bakwai Yehohiyada ya nuna ƙarfinsa. Ya yi alkawari da shugabanni
na ɗari-ɗari, Azariya ɗan Yeroham, Ishmayel ɗan Yehohanan, Azariya ɗan Obed,
Ma’asehiya ɗan Adahiya, da Elishafat ɗan Zikri. 2 Suka ratsa cikin Yahuda suka
tattara Lawiyawa da shugabannin iyalan Isra’ilawa daga dukan garuruwa. Sa’ad da
suka zo Urushalima, 3 dukan taron suka yi alkawari da sarki a haikalin Allah.

Yehohiyada ya ce musu, “Ɗan sarki zai yi mulki yadda UBANGIJI ya yi alkawari
game da zuriyar Dawuda. 4 Yanzu ga abin da za ku yi, shi ne, kashi ɗaya bisa uku na
firistoci da Lawiyawa waɗanda za su yi aiki a Asabbaci su yi tsaro a ƙofofi, 5 kashi
ɗaya bisa ukunku a fadan sarki, kashi ɗaya bisa uku kuma, a Kofar Harsashi, sai
kuma dukan sauran mutane su kasance a filayen haikalin UBANGIJI. 6 Babu wanda
zai shiga haikalin UBANGIJI sai firistoci da Lawiyawan da suke a aiki; za su iya shiga
domin su tsarkaku ne, amma sauran mutane za su kiyaye abin da UBANGIJI ya sa
su yi. 7 Lawiyawa za su tsaya kewaye da sarki, kowane mutum da makamansa a
hannunsa. Duk wanda ya shiga haikali sai a kashe shi. Ku tsaya kusa da sarki a duk
inda ya tafi.”

8 Lawiyawa da dukan mutanen Yahuda suka yi yadda Yehohiyada firist ya umarta.
Kowanne ya ɗauki mutanensa, waɗanda suke aiki a Asabbaci da waɗanda suka
gama aiki, gama Yehohiyada firist bai bar waɗansu ɓangarori ba. 9 Sa’an nan ya
ba shugabannin māsu da garkuwoyi manya da ƙanana na sarki Dawuda, waɗanda
suke cikin haikalin Allah. 10 Ya kuma sa dukan mutane, kowanne da makaminsa a
hannunsa, kewaye da sarki, kusa da bagade da kuma haikali, daga gefen kudu zuwa
gefen arewa na haikali.

11 Yehohiyada da ’ya’yansa maza suka fitar da ɗan sarki suka sa rawani a kansa;
suka miƙa masa alkawarin, suka kuma yi shelarsa a matsayin sarki. Suka shafe shi
suka kuma tā da murya suna cewa, “Ran sarki yă daɗe!”

12 Sa’ad da Ataliya ta ji surutun mutane suna gudu suna yabon sarki, sai ta
tafi wurinsu a haikalin UBANGIJI. 13 Ta duba, a can kuwa ga sarki, tsaye kusa da
ginshiƙinsa a mashigi. Manyan sojoji da masu bushe-bushe suna kusa da sarki, dukan
mutanen ƙasar kuwa suna farin ciki suna busa ƙahoni, mawaƙa kuma da kayan kiɗi
suna bi da yabo. Sai Ataliya ta yage rigunanta ta yi ihu tana cewa, “Cin amanar ƙasa!
Cin amanar ƙasa!”

14 Yehohiyada firist ya fito da shugabanni waɗanda suke shugabancin rundunar
sojoji, ya ce musu, “Ku fitar da ita tsakanin sojoji ku kuma kashe duk wanda ya bi ta
da takobi.” Gama firist ya ce, “Kada ku kashe ta a haikalin UBANGIJI.” 15 Saboda haka
suka kama ta yayinda take kaiwa mashigin Kofar Doki a filin fada, a can suka kashe
ta.

16 Sa’an nan Yehohiyada ya yi alkawari cewa shi da mutane da kuma sarki za su
zama mutanen UBANGIJI. 17 Dukan mutane suka tafi haikalin Ba’al suka rurrushe shi.
Suka farfashe bagadan da gumakan, suka kuma kashe Mattan firist na Ba’al a gaban
bagadan.
18 Sa’an nan Yehohiyada ya sa aikin lura da haikalin UBANGIJI a hannuwan firistoci,
waɗanda suke Lawiyawan da Dawuda ya ba su aikin haikali don su miƙa hadayun
ƙonawa na UBANGIJI kamar yadda yake a rubuce a Dokar Musa, da farin ciki da kuma
rerawa, kamar yadda Dawuda ya umarta. 19 Ya kuma sa matsaran ƙofofi a ƙofofin
haikalin UBANGIJI don kada wani da ba shi da tsarki yă shiga.
20 Ya ɗauki shugabannin ɗari-ɗari, manyan gari, shugabannin mutane da dukan
mutanen ƙasar tare da shi ya saukar da sarki daga haikalin UBANGIJI. Suka shiga fada
ta Kofar Bisa suka kuma zaunar da sarki a kujerar sarauta, 21 sai dukan mutanen
ƙasar suka yi farin ciki. Birnin kuwa ya samu zaman lafiya domin an kashe Ataliya
da takobi.

# 24

*Yowash ya yi gyare-gyaren haikali*
*(2 Sarakuna 12.1-16)*

1 Yowash yana da shekara goma sha bakwai sa’ad da ya zama sarki, ya kuma
yi sarauta a Urushalima shekara arba’in. Sunan mahaifiyarsa Zibiya ce; ita daga
Beyersheba. 2 Yowash ya yi abin da yake daidai a gaban UBANGIJI duka shekarun
Yehohiyada firist. 3 Yehohiyada ya zaɓi mata biyu dominsa, yana kuma da ’ya’ya
maza da ’ya’ya mata.
4 Wani lokaci daga baya Yowash ya yanke shawara yă gyara haikalin UBANGIJI. 5 Ya
tara firistoci da Lawiyawa wuri ɗaya ya ce musu, “Ku je garuruwan Yahuda ku karɓa
kuɗin da ya kamata a biya shekara-shekara daga dukan Isra’ila, don gyaran haikalin
Allahnku. Ku yi haka yanzu.” Amma Lawiyawa ba su yi haka nan da nan ba.
6 Saboda haka sarki ya kira Yehohiyada babban firist ya ce masa, “Me ya sa ba ka
bukaci Lawiyawa su kawo harajin da Musa bawan UBANGIJI ya ce a biya daga Yahuda
da Urushalima da kuma taron Isra’ila domin Tentin Sujada Shaida ba?”
7 Yanzu ’ya’ya muguwar macen nan Ataliya maza sun fasa zuwa cikin haikalin
Allah, suka kuma yi amfani da kayayyaki masu tsarki ma wa Ba’al.
8 Bisa ga umarnin sarki, aka yi akwati aka sa a waje, a mashigin haikalin UBANGIJI.
9 Aka yi umarni a Yahuda da Urushalima cewa ya kamata suka kawo wa UBANGIJI
harajin da Musa bawan Allah ya bukaci daga Isra’ila a hamada. 10 Dukan hafsoshi
da dukan mutane suka kawo nasu kuɗin da aka sa musu da farin ciki, suna zuba
su cikin akwatin sai da ya cika. 11 Duk sa’ad da Lawiyawa suka fito da akwatin
zuwa ga hafsoshin sarki, suka kuma ga cewa akwatin yana da kuɗi mai yawa, sai
magatakardan fada da hafsan babban firist su zo su juya kuɗin daga akwatin su mai
da shi wurinsa. Sun riƙa yin haka kullum suka tara kuɗi mai yawa. 12 Sarki da
Yehohiyada suka ba da shi ga mutanen da suka yi aikin da ake bukata don haikalin
UBANGIJI. Suka ɗauki masu gini da kafintoci don su gyara haikalin UBANGIJI, da kuma
ma’aikatan ƙarafa da tagulla don su gyara haikalin.
13 Mutanen da suke lura da aikin natsattsu ne, kuma gyare-gyaren suka ci gaba a
ƙarƙashinsu. Suka sāke gina haikalin Allah bisa ga ainihin fasalinsa suka ƙara masa
ƙarfi. 14 Da suka gama, suka kawo sauran kuɗin wa sarki da Yehohiyada, da su ne
kuwa aka yi kayayyaki domin hidima da kuma domin hadayun ƙonawa, haka kuma
kwanoni da sauran kayayyakin zinariya da azurfa. Muddin Yehohiyada yana raye,
aka riƙa kawo hadayun ƙonawa a haikalin UBANGIJI.

15 Yanzu Yehohiyada ya tsufa kuma cike da shekaru, ya kuwa mutu yana da shekara
ɗari da talatin. 16 Aka binne shi tare da sarakuna a cikin Birnin Dawuda, saboda
kirkin da ya yi a Isra'ila wa Allah da haikalinsa.

### *Muguntar Yowash*

17 Bayan mutuwar Yehohiyada, hafsoshin Yahuda suka zo suka yi mubaya'a wa
sarki, ya kuma saurare su. 18 Suka yashe haikalin UBANGIJI Allah na kakanninsu,
suka bauta wa ginshiƙan Ashera da kuma gumaka. Saboda laifinsu, fushin Allah ya
sauko a kan Yahuda da Urushalima. 19 Ko da yake UBANGIJI ya aiki annabawa zuwa
wurin mutane don su dawo da su gare shi, kuma ko da yake sun ba da shaida a
kansu, ba su saurara ba.
20 Sai Ruhun Allah ya sauko a kan Zakariya ɗan Yehohiyada firist. Ya tsaya a gaban
mutane ya ce, "Ga abin da Allah ya ce, 'Me ya sa ba ku yi biyayya da umarnan
UBANGIJI ba? Ba za ku yi nasara ba. Domin kun yashe UBANGIJI, shi ma ya yashe
ku.' "
21 Amma suka yi masa maƙarƙashiya, kuma ta wurin umarnin sarki suka jajjefe shi
da duwatsu har ya mutu a filin haikalin UBANGIJI. 22 Sarki Yowash bai tuna da alherin
da Yehohiyada mahaifin Zakariya ya nuna masa ba, sai ya kashe ɗansa, wanda ya ce
yayinda yake mutuwa, "Bari UBANGIJI yǎ dubi wannan yǎ kuma sāka maka."
23 Da shekara ta kewaye, mayaƙan Aram suka yi gāba da Yowash suka kai hari
wa Yahuda da Urushalima suka kuma kashe dukan shugabannin mutane, suka
aika da dukan ganima zuwa ga sarkinsu a Damaskus. 24 Ko da yake mayaƙan
Arameyawa sun zo da mutane kaɗan kawai, UBANGIJI ya sa suka ci nasara a kan
sojojin Yahuda mafi yawa, don mutanen Yahuda sun rabu da UBANGIJI Allah na
kakanninsu, aka kuma hukunta Yowash. 25 Sa'ad da Arameyawa suka janye, suka
bar Yowash da mummunan rauni. Hafsoshinsa suka haɗa baki a kansa saboda kisan
ɗan Yehohiyada firist da ya yi, suka kashe shi a kan gadonsa. Ta haka ya mutu aka
kuma binne shi makabartan sarakuna.
26 Waɗanda suka haɗa bakin kuwa su ne Zabad ɗan Shimeyat wata mutuniyar
Ammon da Yehozabad ɗan Shimrit wata mutuniyar Mowab. 27 Labarin 'ya'yansa
maza, annabce-annabce masu yawa game da shi, da tarihin gyaran haikalin Allah
suna a rubuce a rubuce-rubuce a littafin sarakuna. Amaziya ɗansa kuwa ya gāje shi
a matsayin sarki.

# 25

### *Amaziya sarkin Yahuda*
*(2 Sarakuna 14.1-6)*

1 Amaziya yana da shekara ashirin da biyar sa'ad da ya zama sarki, ya kuma yi
mulki a Urushalima shekara ashirin da tara. Sunan mahaifiyarsa Yehoyaddin ce; ita
daga Urushalima ne. 2 Ya yi abin da yake daidai a gaban UBANGIJI, amma ba da dukan
zuciyarsa ba. 3 Bayan sarauta ta kahu a ƙarƙashinsa, sai ya kashe hafsoshin da suka
kashe mahaifinsa sarki. 4 Duk da haka bai kashe 'ya'yansu maza ba amma ya yi
bisa ga abin da yake a rubuce a cikin Doka, a cikin Littafin Musa, inda UBANGIJI ya
umarta, "Ba za a kashe iyaye saboda 'ya'yansu ba; ba kuwa za a kashe 'ya'ya saboda
iyayensu ba; kowa zai mutu saboda zunubansa ne."*

*(2 Sarakuna 14.7)*

5 Amaziya ya tattara mutanen Yahuda ya kuma ba su aiki bisa ga iyalansu, ya ba
da aiki ga shugabannin dubu-dubu da shugabannin ɗari-ɗari, a dukan Yahuda da
Benyamin. Ya kuma tattara waɗanda suke 'yan shekara ashirin da haihuwa ko fiye
ya sami mutane dubu ɗari uku da suke a shirye don aikin soja, da suka isa riƙe māshi

* **25:4** M Sh 24.16.

da garkuwa. 6 Ya kuma ɗauko sojan haya jarumawa dubu ɗari ɗaya daga Isra'ila a
kan talenti ɗari na azurfa.
7 Amma mutumin Allah ya zo wurinsa ya ce, "Ya sarki, waɗannan runduna daga
Isra'ila ba za su tafi tare da kai ba, gama Ubangiji ba ya tare da Isra'ila, ba ya nan
da wani cikin mutanen Efraim. 8 Ko da ma ya tafi ya yi faɗa da ƙwazo a cikin yaƙi,
Allah zai tumɓuke shi a gaban abokan gāba, gama Allah yana da iko yǎ taimaka ko
yǎ tumɓuke."
9 Amaziya ya tambayi mutumin Allah ya ce, "Amma game da talenti ɗarin da na
biya saboda waɗannan rundunonin Isra'ila fa?"
Mutumin Allah ya amsa, "Ubangiji zai ba ka fiye da wannan."
10 Saboda haka Amaziya ya sallame rundunonin da suka zo daga Efraim, ya kuma
mayar da su gida. Suka husata da Yahuda suka koma gida da fushi sosai.
11 Sa'an nan Amaziya ya yi ƙarfin hali ya jagoranci mayaƙansa zuwa Kwarin
Gishiri, inda ya kashe mutanen Seyir dubu goma. 12 Mayaƙan Yahuda suka kuma
kama mutane dubu goma da rai, suka ɗauke su zuwa ƙwanƙolin dutsen, suka yi ta
tunkuɗa su ƙasa suka yi kaca-kaca.
13 Ana cikin haka, sai rundunar da Amaziya ya mai da su gida, waɗanda ba a bari
suka tafi yaƙin ba, suka kai wa garuruwan Yahuda daga Samariya zuwa Bet-Horon
hari. Suka kashe mutane dubu uku suka kwashe ganima mai yawan gaske.
14 Da Amaziya ya dawo daga kisan mutanen Edom, sai ya dawo da allolin mutanen
Seyir. Ya kafa su a matsayin allolinsa, ya rusuna musu, ya kuma miƙa musu hadayun
ƙonawa. 15 Fushin Ubangiji ya yi ƙuna a kan Amaziya, sai ya aiki wani annabi
wurinsa wanda ya ce, "Me ya sa ka nemi shawarar allolin mutanen nan, waɗanda
ba za su cece mutanensu daga hannunka ba?"
16 Tun yana cikin magana, sai sarki ya ce masa, "Yaushe muka naɗa ka mai ba
sarki shawara? Rufe mana baki! Me zai hana a kashe ka?"
Sai annabin ya yi shiru, amma ya ce, "Na dai sani Allah ya riga ya shirya zai hallaka
ka, saboda ka aikata wannan, ba ka kuma saurari shawarata ba."

*(2 Sarakuna 14.8-14)*

17 Bayan Amaziya sarkin Yahuda ya nemi shawara mashawartansa, sai ya
kalubalanci Yowash ɗan Yehoyahaz, ɗan Yehu, sarkin Isra'ila, "Zo mu gamu fuska
da fuska."
18 Amma Yowash sarkin Isra'ila ya amsa wa Amaziya sarkin Yahuda ya ce, "Wata
ƙaya ce a Lebanon, ta aika da saƙo wa itacen al'ul na Lebanon cewa, 'Ka ba ɗana
'yarka aure.' Sai wani naman jeji na Lebanon ya zo ya tattake ƙayar. 19 Ka ce wa
kanka cewa ka ci Edom da yaƙi, yanzu kuwa kana fariya da ɗaga kai. Amma tsaya
dai a gida! Me ya sa kake neman faɗa kana neman fāɗuwarka da ta Yahuda?"
20 Amma Amaziya bai saurara ba gama Allah ya yi haka domin yǎ miƙa su ga
Yehowash, domin sun nemi shawarar allolin Edom. 21 Saboda haka Yowash sarkin
Isra'ila ya kai yaƙi. Shi da Amaziya sarkin Yahuda suka fuskanci juna a Bet-
Shemesh a Yahuda. 22 Isra'ila ta fatattaki Yahuda, sai kowane mutum ya gudu
zuwa gidansa. 23 Yehowash sarkin Isra'ila ya kama Amaziya sarkin Yahuda, ɗan
Yowash, ɗan Ahaziya a Bet-Shemesh. Sa'an nan Yehowash ya kawo shi Urushalima
ya farfasa katangar Urushalima daga Kofar Efraim har zuwa Kofar Kusurwa, wani
sashe mai tsawon ƙafa ɗari shida. 24 Ya kwashe dukan zinariya da azurfa da dukan
kayayyakin da aka samu a haikalin Allah waɗanda suke a ƙarƙashin kulawar Obed-
Edom, da kaya masu daraja na gidan sarki, da waɗanda aka kamo cikin yaƙi, ya
kawo Samariya.

*(2 Sarakuna 14.15-20)*

25 Amaziya ɗan Yowash sarkin Yahuda ya rayu shekara goma sha biyar bayan
mutuwar Yehowash ɗan Yehoyahaz sarkin Isra'ila. 26 Game da sauran ayyukan

mulkin Amaziya, daga farko zuwa ƙarshe, an rubuta su a littafin sarakunan Yahuda
da Isra'ila. 27 Sa'ad da Amaziya ya bar bin UBANGIJI, aka shirya masa maƙarƙashiya
a Urushalima, sai ya gudu zuwa Lakish, amma suka aiki mutane suka bi shi zuwa
Lakish, a can suka kashe shi. 28 Aka dawo da shi a kan doki, aka binne shi tare da
kakanninsa a Birnin Yahuda.

# 26

*Uzziya sarkin Yahuda*
*(2 Sarakuna 14.21,22; 15.1-7)*

1 Sai dukan mutanen Yahuda suka ɗauki Uzziya[*] wanda yake da shekara goma
sha shida da haihuwa, suka naɗa shi sarki a madadin mahaifinsa Amaziya. 2 Shi ne
wanda ya sāke gina Elot ya kuma mai da shi ga Yahuda bayan Amaziya ya huta tare
da kakanninsa.
3 Uzziya yana da shekara goma sha shida sa'ad da ya zama sarki, ya kuma yi
mulki a Urushalima shekara hamsin da biyu. Sunan mahaifiyarsa Yekoliya ce; ita
daga Urushalima ce. 4 Ya yi abin da yake daidai a gaban UBANGIJI, kamar dai yadda
mahaifinsa Amaziya ya yi. 5 Ya nemi Allah a kwanakin Zakariya, wanda ya koyar da
shi a tsoron Allah. Muddin ya nemi UBANGIJI, Allah ya ba shi nasara.
6 Ya yi yaƙi da Filistiyawa ya kuma rushe katangar Gat, Yabne da kuma Ashdod.
Sa'an nan ya sāke gina garuruwa kusa da Ashdod da sauran wurare a cikin
Filistiyawa. 7 Allah ya taimake shi a kan Filistiyawa da kuma a kan Larabawa
waɗanda suke zama a Gur-Ba'al da kuma a kan Meyunawa. 8 Ammonawa suka kawo
haraji wa Uzziya, sunan da ya yi kuwa ya bazu har iyakar Masar, domin ya zama
mai iko sosai.
9 Uzziya ya gina hasumiyoyi a Urushalima a Kofar Kusurwa, a Kofar Kwari da kuma
a kusurwar katanga, ya kuma yi musu katanga. 10 Ya gina hasumiyoyi a hamada ya
kuma haƙa rijiyoyi masu yawa, gama yana da dabbobi masu yawa a gindin duwatsu
da kuma a kwari. Yana da mutane masu yin masa aiki a gonakinsa da gonakin
inabinsa a tuddai da kuma a ƙasashe masu dausayi, gama yana son noma.
11 Uzziya ya kasance da gogaggun mayaƙa, a shirye su fito ɓangarori-ɓangarori
bisa ga yawansu yadda Yehiyel magatakarda, da Ma'asehiya jarumi, suka karkasa
su bisa ga umarnin Hananiya, ɗaya daga cikin fadawa. 12 Yawan shugabannin
iyali a bisa jarumawa sun kai 2,600. 13 A ƙarƙashin shugabancinsu akwai mayaƙa
307,500 horarru don yaƙi, mayaƙa masu ƙarfi don su taimaki sarki a kan abokan
gābansa. 14 Uzziya ya tanada garkuwoyi, māsu, hulunan kwano, kayan sulke, baka da
majajjawa don mayaƙan gaba ɗaya. 15 A Urushalima ya yi na'urori da gwanaye suka
sarrafa don amfani a hasumiyoyi da kuma a kusurwar kāriya don harbin kibiyoyi da
jefan manyan duwatsu. Sunansa ya bazu ko'ina, gama ya sami taimako sosai har ya
zama mai iko.
16 Amma bayan Uzziya ya zama mai iko, sai ɗaga kai ya kai shi ga fāɗuwa. Bai yi
aminci ga UBANGIJI Allahnsa ba, ya kuma shiga haikalin UBANGIJI don yǎ ƙone turare a
bagaden turare. 17 Azariya firist tare da waɗansu firistoci tamanin na UBANGIJI masu
ƙarfin hali suka bi shi ciki. 18 Suka kalubalance shi suka ce, "Ba daidai ba ne, Uzziya,
ka ƙone turare ga UBANGIJI. Wannan aikin firistoci zuriyar Haruna ne, waɗanda aka
tsarkake don ƙone turare. Ka bar wuri mai tsarki, gama ka kasance marar aminci;
kuma UBANGIJI Allah ba zai girmama ka ba."
19 Uzziya wanda yake da farantin wuta a hannunsa a shirye don ƙone turare, ya
husata. Yayinda yake fushi da firistocin a gabansu a gaban bagaden turare a haikalin
UBANGIJI, sai kuturta ta faso a goshinsa. 20 Sa'ad da Azariya babban firist da dukan

* **26:1** Ana kuma kira shi Azariya

sauran firistoci suka dube shi, sai suka ga cewa yana da kuturta a goshinsa, saboda
haka suka gaggauta tunkuɗa shi waje nan da nan. Tabbatacce, shi kansa ma ya yi
marmari yǎ bar wurin domin Ubangiji ya buge shi.
21 Sarki Uzziya ya kasance da kuturta har ranar mutuwarsa. Ya zauna a gidan da
aka ware, da kuturci, aka kuma ware shi daga haikalin Ubangiji. Yotam ɗansa ya
lura da fadan ya kuma yi mulkin mutanen ƙasar.
22 Sauran ayyukan mulkin Uzziya daga farko zuwa ƙarshe, suna a rubuce ta
hannun annabi Ishaya ɗan Amoz. 23 Uzziya ya huta da kakanninsa aka kuma binne
shi kusa da su a fili don binnewar da take ta sarakuna, domin mutane sun ce, “Yana
da kuturta.” Sai Yotam ɗansa ya gāje shi a matsayin sarki.

# 27

*Yotam sarkin Yahuda*
*(2 Sarakuna 15.32-38)*

1 Yotam yana da shekara ashirin da biyar sa’ad da ya zama sarki, ya kuma yi mulki
a Urushalima shekara goma sha shida. Sunan mahaifiyarsa Yerusha, ’yar Zadok. 2 Ya
yi abin da yake daidai a gaban Ubangiji, kamar yadda mahaifinsa Uzziya ya yi, sai
dai bai kutsa cikin haikalin Ubangiji kamar mahaifinsa ba. Mutane kuwa, suka ci
gaba da aikata ayyukan lalaci. 3 Yotam ya sāke ginin Kofar Bisa na haikalin Ubangiji,
ya kuma yi aiki sosai a katanga a tudun Ofel. 4 Ya gina garuruwa a tuddan Yahuda,
ya giggina katanga da gine-gine masu tsawo a wuraren da suke a kurmi.
5 Yotam ya yi yaƙi da sarkin Ammonawa ya kuma ci su. A wannan shekara
Ammonawa suka biya shi haraji talenti ɗari na azurfa, garwan alkama dubu goma
da kuma garwa dubu goma na sha’ir. Ammonawa suka kawo masa wannan kuma a
shekara ta biyu da ta uku.
6 Yotam ya ƙaru a iko saboda ya daidaita al’amuransa a gaban Ubangiji Allahnsa.
7 Sauran ayyuka a mulkin Yotam, haɗe da dukan yaƙe-yaƙensa da waɗansu
abubuwan da ya yi, suna a rubuce a littafin sarakunan Isra’ila da na Yahuda. 8 Yana
da shekara ashirin da biyar sa’ad da ya zama sarki, ya kuma yi mulki a Urushalima
shekara goma sha shida. 9 Yotam ya huta tare da kakanninsa, aka kuma binne shi a
Birnin Dawuda. Sai Ahaz ɗansa ya gāje shi a matsayin sarki.

# 28

*Ahaz sarkin Yahuda*
*(2 Sarakuna 16.1-4)*

1 Ahaz yana da shekara ashirin sa’ad da ya zama sarki, ya kuma yi mulki a
Urushalima shekara goma sha shida. Ba kamar Dawuda kakansa ba, bai yi abin
da yake daidai a gaban Ubangiji ba. 2 Ya yi tafiya a hanyoyin sarakunan Isra’ila ya
kuma yi zubin gumaka domin a bauta wa Ba’al. 3 Ya ƙone hadayu a Kwarin Ben
Hinnom, ya kuma miƙa ’ya’yansa maza a cikin wuta, yana bin hanyoyi banƙyama
na al’umman da Ubangiji ya kora a gaban Isra’ilawa. 4 Ya miƙa hadayu, ya kuma
ƙone turare a masujadan kan tudu, a bisa tuddai da kuma ƙarƙashin kowane itace
mai inuwa.

*(2 Sarakuna 16.1-4)*

5 Saboda haka Ubangiji Allahnsa ya miƙa shi ga sarkin Aram. Arameyawa suka ci
shi a yaƙi, suka kuma kwashe mutanensa da yawa a matsayin ’yan kurkuku, suka
kawo Damaskus.

Ya kuma ba da shi ga sarkin Isra’ila, wanda ya jijji masa a yaƙi. 6 A rana ɗaya Feka
ɗan Remaliya ya kashe sojoji dubu ɗari da dubu ashirin a Yahuda, domin Yahuda
sun yashe Ubangiji Allah na kakanninsu. 7 Zikri, wani jarumin Efraim, ya kashe

Maʼasehiya ɗan sarki, Azrikam hafsa mai lura da fada, da kuma Elkana, mataimakin
sarki. 8 Israʼilawa suka kame kamammu daga ʼyanʼuwansu mata, ʼyaʼya maza da
kuma ʼyaʼya mata dubu ɗari biyu. Suka kuma kwashe ganima mai yawan gaske,
waɗanda suka kwasa zuwa Samariya.

9 Amma wani annabin Ubangiji mai suna Oded yana a can, sai ya fito don yă sadu
da mayaƙa saʼad da suke komowa zuwa Samariya. Ya ce musu, “Domin Ubangiji
Allah na kakanninku yana fushi da Yahuda, ya ba da su cikin hannunku. Sai kuka
kashe su cikin fushin da ya kai sama. 10 Yanzu kuma kuna niyya ku mai da maza
da matan Yahuda da Urushalima bayinku. Amma ku ɗin ba ku da laifin zunubi ga
Ubangiji Allahnku ne? 11 To, ku saurare ni! Ku mai da ʼyanʼuwanku da kuka kama a
matsayin ʼyan kurkuku, gama fushin Ubangiji yana a kanku.”

12 Sai waɗansu shugabanni a Efraim, Azariya ɗan Yehohanan, Berekiya ɗan
Meshillemot, Hezekiya ɗan Shallum da Amasa ɗan Hadlai, suka tasar wa waɗanda
suke isowa daga yaƙi. 13 Suka ce, “Dole ku kawo waɗannan ʼyan kurkukun a nan,
ko kuwa za ku yi laifi a gaban Ubangiji. Kuna niyya ku ƙara ga zunubinmu da kuma
laifinmu? Gama laifinmu ya riga ya yi yawa, kuma fushinsa mai tsanani yana a kan
Israʼila.”

14 Saboda haka sojoji suka ba da ʼyan kurkukun da ganima a gaban hafsoshi da
dukan taron. 15 Sai mutanen da aka kira sunansu suka tashi, suka ɗauki kamammun,
da ganimar, suka sa wa dukan waɗanda suke tsirara sutura. Suka sa musu sutura,
suka ba su takalma, suka ba su abinci da abin sha, suka shafa musu mai. Suka
hawar da dukan raunana a kan jakuna, suka kai su wurin ʼyanʼuwansu a Yeriko,
wato, Birnin Itatuwan Dabino, saʼan nan suka koma Samariya.

*(2 Sarakuna 16.7-9)*

16 A lokacin nan Sarki Ahaz ya aika wurin sarkin Assuriya neman taimako.
17 Mutanen Edom sun sāke zuwa suka yaƙi Yahuda suka kuma kwashe ʼyan kurkuku,
18 yayinda Filistiyawa suka kai hari wa garuruwa a gindin tuddai da kuma a Negeb
na Yahuda. Suka kame su suka kuma zauna a Bet-Shemesh, Aiyalon da Gederot, haka
ma Soko, Timna da Gimzo tare da ƙauyuka kewayensu. 19 Ubangiji ya ƙasƙantar da
Yahuda saboda Ahaz sarkin Isra'ila,* gama ya hadasa mugunta a Yahuda kuma ya
kasance marar aminci ga Ubangiji. 20 Tiglat-Fileser† sarkin Assuriya ya zo wurinsa,
sai ya wahalar da sarki Ahaz maimakon taimakonsa. 21 Ahaz ya ɗauki waɗansu
abubuwa daga haikalin Ubangiji da kuma daga fadan sarki da kuma daga sarakuna,
ya ba da su ga sarkin Assuriya, amma wannan bai taimake shi ba.

22 Cikin lokacin wahalarsa Sarki Ahaz ya ƙara zama marar aminci ga Ubangiji. 23 Ya
miƙa hadayu ga allolin Damaskus, waɗanda suka ci shi a yaƙi; gama ya yi tunani,
“Da yake allolin sarakunan Aram sun taimake su, zan miƙa hadayu domin su taimake
ni.” Amma suka zama sanadin fāɗuwarsa da kuma fāɗuwar dukan Isra'ila.
24 Ahaz ya tattara kayayyaki daga haikalin Allah ya kwashe su. Ya kulle ƙofofin
haikalin Ubangiji ya kakkafa bagadai a kowace kusurwa a titin Urushalima. 25 A
kowane gari a Yahuda, ya gina masujadan kan tudu don ƙone hadayu ga waɗansu
alloli, ya kuma tsokane Ubangiji Allah na kakanninsa ya yi fushi.

26 Sauran ayyukan mulkinsa da dukan hanyoyinsa, daga farko zuwa ƙarshe, suna
a rubuce a littafin sarakunan Yahuda da Isra'ila. 27 Ahaz ya huta tare da kakanninsa,
aka kuma binne shi a birnin Urushalima, amma ba a sa shi a makabartan sarakunan
Isra'ila ba. Sai Hezekiya ɗansa ya gāje shi a matsayin sarki.

---

* **28:19** Wato, Yahuda, yadda yake sau da sau a 2 Tarihi † **28:20** Da Ibraniyanci Tilgat-Filneser, wani sunan na Tiglat-Fileser.

# 29

*Hezekiya ya tsarkake haikali*
*(2 Sarakuna 18.1-3)*

1 Hezekiya yana da shekara ashirin da biyar sa'ad da ya zama sarki, ya kuma
yi mulki a Urushalima shekara ashirin da tara. Sunan mahaifiyarsa Abiya, 'yar
Zakariya. 2 Ya yi abin da yake daidai a gaban UBANGIJI, kamar dai yadda kakansa
Dawuda ya yi.

3 A wata na farkon a farkon shekarar mulkinsa, ya buɗe ƙofofin haikalin UBANGIJI
ya gyara su. 4 Ya kawo firistoci da Lawiyawa, ya tattara su a filin da yake a gefen
gabas 5 ya kuma ce musu, "Ku saurare ni, Lawiyawa! Ku tsarkake kanku yanzu,
ku kuma tsarkake haikalin UBANGIJI Allah na kakanninku. Ku fid da ƙazanta daga
wuri mai tsarki. 6 Kakanninku ba su yi aminci ba; suka aikata abin da yake mugu a
gaban UBANGIJI Allahnmu, suka kuma yashe shi. Suka juya fuskokinsu daga mazaunin
UBANGIJI suka kuma juya masa baya. 7 Suka kulle ƙofofin shirayi, suka kuma kashe
fitilu. Ba su ƙone turare ko su miƙa hadayun ƙonawa a wuri mai tsarki ga Allah na
Isra'ila ba. 8 Saboda haka, fushin UBANGIJI ya fāɗo a kan Yahuda da Urushalima; ya
mai da su abin tsoro da abin banrazana da kuma abin ba'a, kamar yadda kuke gani
da idanunku. 9 Abin da ya sa ke nan kakanninmu suka fāɗi ta takobi, kuma shi ya sa
aka kai 'ya'yanmu maza da 'ya'yanmu mata da matanmu bauta. 10 Yanzu ina niyya
in yi alkawari da UBANGIJI, Allah na Isra'ila, domin fushinsa yă kauce daga gare mu.
11 'Ya'yana maza, kada ku yi sakaci yanzu, gama UBANGIJI ya zaɓe ku don ku tsaya a
gabansa ku kuma yi masa hidima, don ku yi hidima a gabansa ku kuma ƙone turare."

12 Sai waɗannan Lawiyawa suka shiga aiki,

daga Kohatawa
Mahat ɗan Amasai da Yowel ɗan Azariya.
Daga Kabilar Merari,
Kish ɗan Abdi da Azariya ɗan Yahallelel.
Daga Gershonawa,
Yowa ɗan Zimma da Eden ɗan Yowa.
13 Daga zuriyar Elizafan,
Shimri da Yehiyel.
Daga zuriyar Asaf,
Zakariya da Mattaniya.
14 Daga iyalin Heman,
Yehiyel da Shimeyi.
Daga zuriyar Yedutun,
Shemahiya da Uzziyel.

15 Da suka tattara 'yan'uwansu suka kuma tsarkake kansu, sai suka shiga ciki suka
tsarkake haikalin UBANGIJI, kamar yadda sarki ya umarta, suna bin maganar UBANGIJI.
16 Firistoci suka shiga cikin wuri mai tsarki na UBANGIJI suka tsarkake shi. Suka fitar
da dukan abin da yake marar tsabta da suka samu a haikalin UBANGIJI zuwa filin
haikalin UBANGIJI. Lawiyawa suka ɗauke su suka kai su Kwarin Kidron. 17 Suka fara
tsarkakewar a rana ta farko na farkon wata, a rana ta takwas na watan kuwa suka
kai shirayin UBANGIJI. Karin kwana takwas kuma suka tsarkake haikalin UBANGIJI
kansa, suka gama a rana ta goma sha shida na farkon wata.

18 Sa'an nan suka tafi wurin Sarki Hezekiya suka faɗa masa, "Mun tsarkake haikalin
UBANGIJI gaba ɗaya, bagaden ƙone hadaya tare da dukan kayayyakinsa, da tebur don

shirya tsarkaken burodi, tare da dukan kayayyakinsa. [19] Mun shirya muka kuma
tsarkake dukan kayayyakin da Sarki Ahaz ya cire cikin rashin amincinsa yayinda
yake sarki. Yanzu suna a gaban bagaden UBANGIJI.”
[20] Da sassafe kashegari Sarki Hezekiya ya tattara manyan birni wuri ɗaya, suka
haura zuwa haikalin UBANGIJI. [21] Suka kawo bijimai bakwai, raguna bakwai,
bunsurai bakwai da kuma awaki mata bakwai a matsayin hadaya don zunubi domin
masarauta, domin wuri mai tsarki da kuma domin Yahuda. Sarki ya umarce firistoci,
zuriyar Haruna, su miƙa waɗannan a bagaden UBANGIJI. [22] Saboda haka suka
yayyanka bijiman, firistoci suka karɓi jinin suka yayyafa a kan bagade. Suka kuma
yanka ragunan suka yayyafa jinin a bagaden. Haka kuma suka yanka ’yan ragunan
suka yayyafa jinin a bagaden. [23] Aka kawo awaki domin hadaya don zunubi a gaban
sarki da taron, suka kuwa ɗibiya hannuwansu a kansu. [24] Sa’an nan firistoci suka
yayyanka awakin suka miƙa jininsu a bagade domin hadaya don zunubi don kafara
saboda dukan Isra’ila, domin sarki ya umarta a yi hadaya ta ƙonawa da hadaya don
zunubi domin dukan Isra’ila.
[25] Sarki Hezekiya ya ajiye Lawiyawa a cikin haikalin UBANGIJI tare da ganguna,
garayu da molaye, yadda Dawuda da Gad mai duba na sarki da kuma annabi Natan
suka tsara. UBANGIJI ne ya umarta wannan ta wurin annabawansa. [26] Saboda haka
Lawiyawa suka tsaya a shirye tare da kayan kiɗin Dawuda, firistoci kuma tare da
ƙahoninsu.
[27] Hezekiya ya ba da umarni a miƙa hadaya ta ƙonawa a kan bagade. Yayinda
aka fara miƙawa, ana rerawa ga UBANGIJI, tare da bushe-bushe da kiɗe-kiɗen kayan
waƙa na Dawuda sarkin Isra’ila. [28] Dukan taron suka durƙusa suka yi sujada, yayinda
mawaƙa suke rerawa, ana kuma busa ƙahoni, dukan wannan ya ci gaba sai da aka
gama miƙa hadaya ta ƙonawa.
[29] Sa’ad da aka gama miƙawa, sai sarki da mutanen da suke tare da shi suka
durƙusa suka yi sujada. [30] Sarki Hezekiya da fadawansa suka umarci Lawiyawa
su yabi UBANGIJI da kalmomin Dawuda da na Asaf mai duba. Saboda haka suka rera
yabai da murna, suka sunkuyar da kawunansu suka yi sujada.
[31] Sa’an nan Hezekiya ya ce, “Yanzu kun keɓe kanku ga UBANGIJI. Ku zo ku kuma
kawo hadayu da hadayun godiya zuwa ga haikalin UBANGIJI.” Saboda haka taron
suka kawo hadayu da hadayun godiya, da kuma dukan waɗanda suke da niyya suka
kawo hadayun ƙonawa.
[32] Yawan hadayun ƙonawan da taron suka kawo, bijimai saba’in ne, raguna ɗari
da kuma bunsurai ɗari biyu, dukansu kuwa domin hadayun ƙonawa ga UBANGIJI
ne. [33] Dabbobin da aka tsarkake a matsayi hadayu sun kai bijimai ɗari shida da
tumaki da kuma awaki dubu uku. [34] Firistoci fa, suka kāsa sosai don fiɗan dukan
dabbobin da za a miƙa don hadayun ƙonawa; saboda haka ’yan’uwansu Lawiyawa
suka taimake su har aka gama aiki kafin sauran firistoci su sami damar tsarkake
kansu. Gama Lawiyawa sun fi firistoci himma wajen tsarkakewar kansu. [35] Aka
kasance da hadayun ƙonawa a yalwace, tare da kitsen hadayun salama da hadayun
sha da suke tafe da hadayun ƙonawa.
Saboda haka aka sāke kafa hidimar haikalin UBANGIJI. [36] Hezekiya da dukan
mutane suka yi farin ciki game da abin da Allah ya yi wa mutanensa, domin ya
faru farat ɗaya.

# 30

*Hezekiya ya yi Bikin Ketarewa*

[1] Sai Hezekiya ya aika wa dukan Isra’ila da Yahuda, ya kuma rubuta wasiƙu zuwa
Efraim da Manasse, yana gayyatarsu su zo haikalin UBANGIJI a Urushalima, su kuma

yi Bikin Ketarewa ga UBANGIJI, Allah na Isra'ila. [2] Sarki da fadawansa da dukan taro
a Urushalima suka yanke shawara su yi Bikin Ketarewa a wata na biyu. [3] Ba su iya
yinsa a daidai lokacinsa ba domin babu isashen firistocin da suka tsarkake kansu,
mutane kuma ba su taru a Urushalima ba. [4] Shirin ya yi kyau ga sarki da kuma
dukan taron. [5] Suka yanke shawara su yi shelar a ko'ina a Isra'ila, daga Beyersheba
zuwa Dan, suna kiran mutane su zo Urushalima, suka kuma yi Bikin Ketarewa ga
UBANGIJI Allah na Isra'ila. Ba a yi bikin da mutane masu yawa bisa ga abin da aka
rubuta ba.

[6] Bisa ga umarnin sarki, sai 'yan aika suka tafi ko'ina a Isra'ila da Yahuda da wasiƙu
daga sarki da kuma daga fadawansa, wasiƙar tana cewa,

"Mutanen Isra'ila, ku dawo ga UBANGIJI Allah na Ibrahim, Ishaku da Isra'ila,
domin yǎ dawo gare ku, ku da kuka tafi, ku da kuka kuɓuce daga hannun sarakuna
Assuriya. [7] Kada ku zama kamar iyayenku da 'yan'uwanku, waɗanda suka yi
rashin aminci ga UBANGIJI Allah na kakanninsu, har ya mai da su abin tsoro,
yadda kuke gani. [8] Kada ku yi taurinkai, yadda iyayenku suka yi; ku miƙa kai
ga UBANGIJI. Ku zo wuri mai tsarki, wanda ya tsarkake har abada. Ku bauta wa
UBANGIJI Allahnku, domin fushi mai zafi yǎ juye daga gare ku. [9] In kuka dawo
wurin UBANGIJI, sa'an nan waɗanda suka kama 'yan'uwanku da 'ya'yanku za su
nuna musu tausayi, su kuma dawo wannan ƙasa, gama UBANGIJI Allahnku mai
alheri ne mai jinƙai kuma. Ba zai kau da fuskarsa daga gare ku ba, in kuka dawo
gare shi."

[10] 'Yan aika suka tafi gari-gari a cikin Efraim da Manasse, har zuwa Zebulun, amma
mutane suka yi musu dariyar reni, suka kuma yi musu ba'a. [11] Duk da haka, waɗansu
mutanen Asher, Manasse da Zebulun suka ƙasƙantar da kansu suka tafi Urushalima.
[12] Haka ma a Yahuda, hannun Allah yana a kan mutane don yǎ ba su zuciya ɗaya su
yi abin da sarki da fadawansa suka umarta, suna bin maganar UBANGIJI.

[13] Taron mutane mai girma ya haɗu a Urushalima don Bikin Burodi Marar Yisti a
wata na biyu. [14] Suka kawar da bagadai a Urushalima suka fid da bagadan turare
suka zubar da su a Kwarin Kidron.

[15] Suka yanka ɗan ragon Bikin Ketarewa a rana ta goma sha huɗu na wata na
biyu. Firistoci da Lawiyawa suka ji kunya suka tsarkake kansu, suka kawo hadayun
ƙonawa a haikalin UBANGIJI. [16] Sa'an nan suka ɗauki matsayinsu na kullum yadda
yake a Dokar Musa mutumin Allah. Firistoci suka yayyafa jinin da Lawiyawa suka ba
su. [17] Da yake da yawa cikin taron ba su tsarkake kansu ba, dole Lawiyawa su yanka
'yan ragunan Bikin Ketarewa domin dukan waɗanda ba su da tsarki, ba su kuma
iya tsarkake ragunansu ga UBANGIJI ba. [18] Ko da yake yawancin mutanen da suka
zo daga Efraim, Manasse, Issakar da Zebulun ba su tsarkake kansu ba, duk da haka
suka ci Bikin Ketarewa, ba tare da bin abin da yake a rubuce ba. Amma Hezekiya
ya yi addu'a dominsu cewa, "Bari UBANGIJI, wanda yake nagari, yǎ gafarta wa kowa
[19] wanda ya sa zuciyarsa ga neman Allah, UBANGIJI Allah na kakanninsa, ko da shi
marar tsarki ne bisa ga dokokin wuri mai tsarki." [20] UBANGIJI kuwa ya ji Hezekiya ya
kuma warkar da mutane.

[21] Isra'ilawan da suka kasance a Urushalima suka yi Bikin Burodi Marar Yisti kwana
bakwai da farin ciki mai girma, yayinda Lawiyawa da firistoci suke rera ga UBANGIJI
kowace rana, haɗe da kayan kiɗin yabon UBANGIJI.

[22] Hezekiya ya yi magana mai ƙarfafawa ga dukan Lawiyawa waɗanda suka nuna
ganewar fasaha a hidimar UBANGIJI. Kwana bakwai suka ci rabonsu da aka tsara,
suka miƙa hadayun salama, suka kuma yabi UBANGIJI Allah na kakanninsu.

[23] Dukan mutanen suka yarda su ƙara kwana bakwai kuma, sai suka ci gaba da
bikin cikin farin ciki har waɗansu kwana bakwai kuma. [24] Hezekiya sarkin Yahuda ya

tanada bijimai dubu ɗaya da tumaki da kuma awaki dubu bakwai wa taron, fadawa
kuma suka tanada musu bijimai dubu da kuma tumaki da awaki dubu goma. Firistoci
masu yawa suka tsarkake kansu. 25 Taron gaba ɗaya na Yahuda suka yi farin ciki,
tare da firistoci da kuma Lawiyawa da dukan waɗanda suka taru daga Isra'ila, har
ma da baƙi waɗanda suka zo daga Isra'ila da waɗanda suke zama a Yahuda. 26 Aka yi
farin ciki mai girma a Urushalima, gama tun zamanin Solomon ɗan Dawuda sarkin
Isra'ila, ba a taɓa yin wani abu kamar haka a Urushalima ba. 27 Firistoci da Lawiyawa
suka tsaya suka albarkace mutane, Allah kuma ya ji su, gama addu'arsu ya kai sama,
mazauninsa mai tsarki.

# 31

*(2 Sarakuna 18.4)*

1 Sa'ad da aka gama dukan wannan, sai Isra'ilawan da suke can suka fita zuwa
garuruwan Yahuda, suka rurrushe keɓaɓɓun duwatsu suka kuma farfashe ginshiƙan
Ashera. Suka rurrushe masujadan kan tudu da bagadai, ko'ina a Yahuda da Benyamin
da kuma cikin Efraim da Manasse. Bayan sun rurrushe dukansu, sai Isra'ilawa suka
koma garuruwansu, kowanne zuwa mahallinsa.

*Tare-tare don sujada*

2 Hezekiya kuma ya raba firistoci da Lawiyawa kashi-kashi, kowanne da hidimarsa,
firistoci da Lawiyawa, don hadayu na ƙonawa da na salama, su yi hidima, su yi
godiya, su kuma rera yabai a ƙofofin mazaunin UBANGIJI. 3 Sarki ya ba da taimako
daga mallakarsa domin hadayun ƙonawa, safe da yamma da kuma don hadayun
ƙonawa a Asabbatai, Sabon Wata da kuma ƙayyadaddun bukukkuwa kamar yadda
yake a rubuce a cikin Dokar UBANGIJI. 4 Ya umarci mutanen da suke zama a
Urushalima su ba da rabon da yake na firistoci da Lawiyawa, don su ƙwallafa ransu
ga Dokar UBANGIJI. 5 Nan da nan aka baza umarnin, sai Isra'ilawa suka bayar 'ya'yan
farin hatsinsu, sabon ruwan inabi, mai da kuma zuma da dukan abin da gona ta
bayar, hannu sake. Suka kawo zakan kowane abu da yawa. 6 Mutanen Isra'ila da
Yahuda waɗanda suke zama a garuruwan Yahuda, su ma suka kawo zakan shanu da
na tumaki da kuma zakan abubuwa masu tsarki da aka keɓe ga UBANGIJI Allahnsu,
suka jibge su tsibi-tsibi. 7 Sun fara yin haka a wata na uku, suka kuma gama a wata
na bakwai. 8 Sa'ad da Hezekiya da fadawansa suka zo suka ga tsibin, sai suka yabi
UBANGIJI, suka kuma albarkace mutanensa Isra'ila.
9 Hezekiya ya tambayi firistoci da Lawiyawa game da tsibin; 10 sai Azariya babban
firist, daga iyalin Zadok ya amsa, "Tun daga lokacin da mutane suka fara kawo
taimakonsu ga haikalin UBANGIJI, muna da isashe don abinci da kuma da yawa da
za mu rage, domin UBANGIJI ya albarkaci mutanensa, saboda haka abin da ya ragu a
rumbu yana da yawa."
11 Hezekiya ya ba da umarni a shirya ɗakunan ajiya a haikalin UBANGIJI, aka kuwa
yi haka. 12 Sa'an nan cikin aminci suka kawo taimako, zakka da keɓaɓɓun kyautai.
Konaniya, wani Balawe, shi ne ke lura da waɗannan abubuwa, kuma ɗan'uwansa
Shimeyi shi ne na biye da shi. 13 Yehiyel, Azaziya, Nahat, Asahel, Yerimot, Yozabad,
Eliyel, Ismakiya, Mahat da Benahiya su ne shugabanni, mataimakan Konaniya da
Shimeyi ɗan'uwansa, waɗanda sarki Hezekiya da Azariya babban shugaban haikalin
Allah suka naɗa.
14 Kore ɗan Imna Balawe, mai tsaron Kofar Gabas, shi ne yake lura da baikon
yardan ran da aka yi wa Allah, don ya karkasa bayarwar da aka keɓe domin
UBANGIJI da hadayu mafi tsarki. 15 Eden, Miniyamin, Yeshuwa, Shemahiya, Amariya
da Shekaniya sun taimake shi da aminci a cikin garuruwan firistoci, suna ba da rabo
wa 'yan'uwansu firistoci bisa ga sassansu, tsofaffi da yara.

[16] Bugu da ƙari, suka ba da rabo ga maza ʼyan shekaru uku ko fiye waɗanda
sunayensu suna a tarihin zuriya, dukan waɗanda ba za su iya shiga haikalin UBANGIJI
su yi ayyukansu na kullum ba, bisa ga nawayarsu da kuma sassansu. [17] Suka kuma
ba da rabo ga firistocin da aka rubuta ta iyalansu cikin tarihin zuriya, haka kuma
ga Lawiyawa masu shekara ashirin ko fiye, bisa ga nawayarsu da kuma sassansu.
[18] Suka haɗa da dukan ƙanana ʼyaʼyansu, mata, da kuma ʼyaʼya maza da ʼyaʼya mata,
alʼumma gaba ɗaya da aka jera a waɗannan tarihin zuriya. Gama sun yi aminci cikin
tsarkake kansu.
[19] Akwai mutane a garuruwa da yawa waɗanda aka sa don su rarraba wa ʼyaʼyan
Haruna, firist, maza, waɗanda suke zaune a gonaki na ƙasar garuruwansu su ba
kowane namijin da aka rubuta na Lawiyawa, rabonsa.
[20] Abin da Hezekiya ya yi ke nan koʼina a Yahuda, yana yin abin da yake da kyau,
daidai da kuma mai aminci a gaban UBANGIJI Allahnsa. [21] Cikin kome da ya yi cikin
hidimar haikalin Allah, cikin biyayya kuma ga doka da umarnai, ya nemi Allahnsa,
ya kuma yi aiki gabagadi. Ta haka kuwa ya yi nasara.

# 32

*Sennakerib ya yi wa Urushalima barazana*
*(2 Sarakuna 18.13-37; Ishaya 36.1-22)*

[1] Bayan dukan abin da Hezekiya ya yi cikin aminci, sai Sennakerib sarkin Assuriya
ya zo ya yaƙi Yahuda. Ya yi kwanto wa biranen katanga, yana zato zai ci su da
yaƙi wa kansa. [2] Saʼad da Hezekiya ya ga Sennakerib ya zo yana kuma niyya yă yaƙi
Urushalima, [3] sai ya yi shawara da fadawansa da hafsoshin mayaƙansa cewa su datse
ruwa daga maɓulɓulan ruwan da yake waje da birnin, suka kuwa taimake shi. [4] Sai
babban taro suka haɗu suka datse dukan maɓulɓulai da rafuffukan da suke gudu
cikin ƙasar. Suka ce "Me zai sa sarakunan Assuriya su zo su sami ruwa barkatai?"
[5] Sai suka yi aiki tuƙuru suna gyaran dukan sassan katangar da suka fāɗi, suna kuma
gina hasumiya a kai. Ya gina wata katanga a waje da wannan, ya kuma ƙara ƙarfin
madogaran gini na Birnin Dawuda. Ya yi makamai masu yawa da kuma garkuwoyi.
[6] Ya naɗa manyan hafsoshi a kan mutane, ya tattara su a gabansa a fili a ƙofar
birni, ya kuma ƙarfafa su da waɗannan kalmomi. [7] "Ku ƙarfafa, ku yi ƙarfin hali.
Kada ku ji tsoro ko ku yi fargaba saboda sarkin Assuriya, da mayaƙan nan masu
yawa da suke tare da shi, gama shi wanda yake tare da mu, ya fi wanda yake tare
da su. [8] Mayaƙa na jiki ne kawai suke tare da shi, amma UBANGIJI Allahnmu ne yake
tare da mu, zai kuwa taimake mu yă kuma yi yaƙinmu." Mutane kuwa suka amince
da maganar Hezekiya, Sarkin Yahuda.
[9] Daga baya, saʼad da Sennakerib sarkin Assuriya da dukan mayaƙansa suke
kwanto wa Lakish, sai ya aiki hafsoshinsa da wannan saƙo wa Hezekiya sarkin
Yahuda da kuma wa dukan mutanen Yahuda waɗanda suke can cewa,
[10] "Ga abin da Sennakerib sarkin Assuriya ya ce ga me kake dogara, har da ka
dāge cikin Urushalima da aka yi mata kwanto? [11] Ai, Hezekiya, ruɗinku yake
yi, don yă sa ku mutu da yunwa da ƙishirwa saʼad da yake ce muku, ʻUBANGIJI
Allahnmu zai cece mu daga hannun sarkin Assuriya.ʼ [12] Hezekiya kansa bai rushe
waɗannan masujadan kan tudu da bagadai, yana ce wa Yahuda da Urushalima,
ʻDole ku yi sujada a gaban bagade guda ku kuma ƙone hadayu a kansa baʼ?
[13] "Ba ku san abin da ni da kuma kakannina suka yi wa dukan mutanen sauran
ƙasashe ba? Allolin ƙasashen nan sun taɓa iya ceton ƙasarsu daga hannuna ne?
[14] Wanne a cikin dukan allolin waɗannan ƙasashe da kakannina suka hallaka ya
taɓa iya ceton mutanensa daga gare ni? To, yaya Allahnku zai iya cetonku daga
hannuna? [15] Yanzu fa, kada ku bar Hezekiya yă ruɗe ku yă kuma ɓad da ku haka.

Kada ku gaskata shi, gama babu allahn wata ƙasa ko masarautar da ya taɓa iya ceton mutanensa daga hannuna ko kuwa hannun kakannina. Balle har Allahnku yă cece ku daga hannuna!”

[16] Hafsoshin Sennakerib suka ci gaba da maganar banza wa UBANGIJI Allah da kuma
a kan bawansa Hezekiya. [17] Sarki ya kuma rubuta wasiƙu yana zagin UBANGIJI, Allah
na Isra'ila, yana faɗin wannan a kansa, “Kamar yadda sauran allolin mutanen sauran ƙasashe ba su iya kuɓutar da mutane daga hannuna ba, haka Allahn Hezekiya ba
zai kuɓutar da mutanensa daga hannuna ba.” [18] Sa'an nan suka yi magana da ƙarfi
cikin Yahudanci wa mutanen Urushalima waɗanda suke kan katanga, don su firgita
su, su kuma sa su ji tsoro don su iya cin birnin. [19] Suka yi magana game da Allah na
Urushalima yadda suka yi game da allolin sauran mutanen duniya, aikin hannuwan mutane.

*(2 Sarakuna 19.14-19,35-37; Ishaya 37.14-20; 37.36-38)*

[20] Sarki Hezekiya da annabi Ishaya ɗan Amoz suka yi kuka cikin addu'a ga sama
game da wannan. [21] Sai UBANGIJI ya aiki mala'ika, wanda ya karkashe dukan jarumawa da shugabanni da kuma hafsoshi a sansanin sarkin Assuriyawa. Saboda haka sai sarkin Assuriya ya janye zuwa ƙasarsa da kunya. Da ya shiga haikalin Allahnsa, sai waɗansu a cikin 'ya'yansa maza suka yanka shi da takobi.

[22] Ta haka UBANGIJI ya ceci Hezekiya da mutanen Urushalima daga hannun Sennakerib sarkin Assuriya da kuma daga hannun dukan sauran. Ya magance su
a kowane gefe. [23] Yawanci mutane suka kawo hadayun ƙonawa zuwa Urushalima wa UBANGIJI da kuma kyautai masu daraja wa Hezekiya sarkin Yahuda. Daga lokacin zuwa gaba dukan ƙasashe suka girmama shi.

### *Girmankai, nasara da kuma mutuwar Hezekiya*
### *(2 Sarakuna 20.1-11; Ishaya 38.1-8)*

[24] A kwanakin nan Hezekiya ya yi ciwo, ya yi kusan mutuwa. Sai ya yi addu'a ga
UBANGIJI, wanda ya amsa masa ya kuma ba shi alama. [25] Amma zuciyar Hezekiya ta yi
girman kai, bai kuwa yi amfani da alherin da aka nuna masa ba, saboda haka fushin
UBANGIJI ya sauko a kansa da kuma a kan Yahuda da Urushalima. [26] Sai Hezekiya ya
tuba daga girma kan zuciyarsa, haka ma mutanen Urushalima; saboda haka fushin UBANGIJI bai zo a kansu a kwanakin Hezekiya ba.

*(2 Sarakuna 20.12-19; Ishaya 39.1-8)*

[27] Hezekiya mai arziki da girma ne ƙwarai, ya kuma yi baitulmali domin azurfa da zinariyarsa da kuma domin duwatsu masu daraja, kayan yaji, garkuwoyi da kuma
domin dukan kayayyaki masu daraja nasa. [28] Ya kuma yi gine-gine domin ajiyar hatsi,
sabon ruwa inabi da mai; ya kuma yi wuraren ajiyar kowane irin shanu dabam-
dabam, da kuma turke domin tumaki. [29] Ya gina ƙauyuka ya kuma samo shanu da garkuna masu yawa, gama Allah ya ba shi arziki mai yawa sosai.

[30] Hezekiya ne ya datse ruwan bisa na maɓulɓular Gihon, ya sa ruwan ya gangara
zuwa gefe yamma na Birnin Dawuda. Ya yi nasara a kome da ya yi. [31] Amma da
masu mulkin Babilon suka aika da jakadu su tambaye shi game alamar da ta faru a ƙasar, Allah ya rabu da shi don yă gwada shi don yă kuma san kome da yake cikin zuciyarsa.

*(2 Sarakuna 20.20,21)*

[32] Sauran ayyukan mulkin Hezekiya da kuma kyawawa ayyukansa, suna a rubuce a cikin wahayin annabi Ishaya ɗan Amoz, a cikin littafin sarakunan Yahuda da
Isra'ila. [33] Hezekiya ya huta tare da kakanninsa, aka kuma binne shi a kan tudu inda makabartan zuriyar Dawuda suke. Dukan Yahuda da kuma mutanen Urushalima suka girmama shi sa'ad da ya mutu. Sai Manasse ɗansa ya gāje shi a matsayin sarki.

# 33

*Manasse sarkin Yahuda*
*(2 Sarakuna 21.1-9,17,18)*

1 Manasse yana da shekara ashirin sa'ad da ya zama sarki, ya kuma yi mulki a
Urushalima shekara hamsin da biyar. 2 Ya yi abin da yake mugu a gaban UBANGIJI,
yana bin ayyukan banƙyama na al'umman da UBANGIJI ya kora a gaban Isra'ilawa.
3 Ya sāke gina masujadan kan tudun da mahaifinsa Hezekiya ya rurrushe; ya tā da
bagadan Ba'al, ya kuma gina ginshiƙan Ashera. Ya rusuna wa dukan rundunonin
taurari, ya kuma yi musu sujada. 4 Ya gina bagadai cikin haikalin UBANGIJI, wanda
UBANGIJI ya ce, "Sunana zai kasance cikin Urushalima har abada." 5 Cikin filayen
haikalin UBANGIJI, ya gina bagadai ga dukan rundunonin taurari. 6 Ya miƙa 'ya'yansa
maza hadaya a wuta cikin Kwarin Ben Hinnom, ya yi bokanci, ya yi duba, ya kuma
yi maitanci, ya nemi shawarar mabiya da masu ruhohi. Ya yi abin da yake mugu
ƙwarai a gaban UBANGIJI, yana tsokanarsa yă yi fushi.

7 Ya ɗauki siffar da aka sassaƙa wadda ya yi, ya sa ta a cikin haikalin Allah, wanda
Allah ya ce wa Dawuda da kuma ɗansa Solomon, "Cikin wannan haikali da kuma
cikin Urushalima, wanda na zaɓa daga cikin kabilan Isra'ila, zan sa Sunana har
abada. 8 Ba zan ƙara bari ƙafafun Isra'ilawa su bar ƙasar da na ba wa kakanninku ba,
in dai suka yi hankali ga yin kome da na umarce su game da duka dokoki, ƙa'idodi da
kuma farillai da na bayar ta wurin Musa." 9 Amma Manasse ya sa Yahuda da mutanen
Urushalima suka kauce, har suka aikata mugunta fiye da al'umman da UBANGIJI ya
hallaka a gaban Isra'ilawa.

10 UBANGIJI ya yi magana da Manasse da mutanensa, amma ba su kula ba.
11 Saboda haka UBANGIJI ya kawo manyan hafsoshin mayaƙan sarkin Assuriya a
kansu, waɗanda suka ɗauki Manasse a matsayi ɗan kurkuku, suka sa ƙugiya a
hancinsa, suka daure shi da sarƙoƙin tagulla suka kuma kai shi Babilon. 12 Cikin
wahalarsa ya nemi tagomashin UBANGIJI Allahnsa ya kuma ƙasƙantar da kansa sosai
a gaban Allah na kakanninsa. 13 Da ya yi addu'a gare shi, sai UBANGIJI ya taɓu da
tubansa, ya kuma saurari roƙonsa; saboda haka ya dawo da shi Urushalima da kuma
zuwa mulkinsa. Sa'an nan Manasse ya san cewa UBANGIJI shi ne Allah.

14 Daga baya ya sāke gina katangar waje na Birnin Dawuda, yamma da maɓulɓular
Gihon a cikin kwari, har zuwa mashigin Kofar Kifi, ya kuma kewaye tudun Ofel; ya
yi ta da tsayi sosai. Ya sa hafsoshin mayaƙa cikin dukan biranen katanga a Yahuda.

15 Ya fid da baƙin alloli, ya kuma fid da siffofi daga haikalin UBANGIJI, haka ma
dukan bagadan da ya gina a kan tudun haikali da kuma cikin Urushalima, ya zubar
da su a bayan birni. 16 Sa'an nan ya gyara bagaden UBANGIJI ya kuma miƙa hadayun
salama da kuma hadayun godiya a bagaden, ya kuma faɗa wa Yahuda su bauta wa
UBANGIJI, Allah na Isra'ila. 17 Mutane dai suka ci gaba da miƙa hadayu a masujadai
kan tudu, amma wa UBANGIJI Allahnsu kaɗai.

18 Sauran ayyukan mulkin Manasse, haɗe da addu'arsa ga Allahnsa da kuma
kalmomin da mai duba ya yi masa cikin sunan UBANGIJI, Allah na Isra'ila, suna a
rubuce cikin tarihin sarakunan Isra'ila.* 19 Addu'arsa da yadda Allah ya taɓu ta
wurin tubansa, da kuma dukan zunubansa da rashin biyayyarsa, da wuraren da
ya gina masujadan kan tudu ya kuma kafa ginshiƙan Ashera da gumaka kafin ya
ƙasƙantar da kansa, duka suna a rubuce cikin tarihin mai duba. 20 Manasse ya huta
tare da kakanninsa, aka kuma binne shi a fadansa. Sai Amon ɗansa ya gāje shi a
matsayin sarki.

* **33:18** Wato, Yahuda, yadda yake sau da sau a 2 Tarihi

*Amon sarki Yahuda*
*(2 Sarakuna 21.19-26)*
21 Amon yana da shekara ashirin da biyu sa'ad da ya zama sarki, ya yi mulki a
Urushalima shekara biyu. 22 Ya yi abin da yake mugu a gaban UBANGIJI kamar yadda
mahaifinsa Manasse ya yi. Amon ya bauta ya kuma miƙa hadayu ga dukan gumakan
da Manasse ya yi. 23 Amma ba kamar mahaifinsa Manasse ba, bai ƙasƙantar da kansa
a gaban UBANGIJI ba; Amon ya ƙara laifinsa.
24 Fadawan Amon sukan yi masa maƙarƙashiya, suka kashe shi a fadansa.
25 Sa'an nan mutanen ƙasar suka kashe dukan waɗanda suka yi wa Sarki Amon
maƙarƙashiya, suka naɗa Yosiya ɗansa sarki a maimakonsa.

# 34

*Gyare-gyaren Yosiya*
*(2 Sarakuna 22.1,2)*
1 Yosiya yana da shekara goma sha takwas sa'ad da ya zama sarki, ya kuma yi mulki
a Urushalima shekara talatin da ɗaya. 2 Ya yi abin da yake daidai a gaban UBANGIJI
ya kuma yi tafiya a hanyoyin kakansa Dawuda, ba tare da juye dama ko hagu ba.
*(2 Sarakuna 23.4-20)*
3 A shekara ta takwas ta mulkinsa, yayinda yake matashi, sai ya fara neman Allah
na kakansa Dawuda. A shekara ta goma sha biyunsa ya fara tsabtacce Yahuda da
Urushalima daga masujadan kan tudu, ginshiƙan Ashera, sassaƙaƙƙun gumaka da
kuma siffofin da aka yi zubi. 4 A ƙarƙashin umarninsa aka rurrushe bagadan Ba'al, ya
kuma tumɓuke bagadan ƙona turare waɗanda suke a bisansu, ya farfashe ginshiƙan
Ashera da kuma sassaƙaƙƙun siffofi. Ya ragargaza waɗannan kucu-kucu, ya barbaɗa
su a kan kaburburan waɗanda suka miƙa musu hadayu. 5 Ya ƙone ƙasusuwan
firistocin gumaka a kan bagaden da a dā suke miƙa hadayunsu, ta haka ya tsabtacce
Yahuda da Urushalima. 6 Ya yi haka cikin garuruwan Manasse, Efraim da Simeyon,
har zuwa Naftali, da kuma cikin kangwayen kewayensu, 7 ya farfashe bagadai da
ginshiƙan Ashera; ya niƙa gumaka suka zama gari, ya kuma yayyanka dukan bagadan
turare kucu-kucu ko'ina a Isra'ila. Sa'an nan ya koma Urushalima.
*(2 Sarakuna 22.3-20)*
8 A shekara ta goma sha takwas ta mulkin Yosiya, ya tsarkake ƙasar da haikalin, ya
aiki Shafan ɗan Azaliya da Ma'asehiya mai mulkin birni, tare da Yowa ɗan Yowahaz,
marubuci, su gyara haikalin UBANGIJI Allah.
9 Suka tafi wurin Hilkiya babban firist suka ba shi kuɗin da aka kawo cikin haikalin
Allah, wanda Lawiyawa masu tsaron ƙofofi sun tattara daga mutanen Manasse,
Efraim da dukan raguwar Isra'ila da kuma daga dukan mutanen Yahuda da Benyamin
da kuma mazaunan Urushalima. 10 Sa'an nan suka danƙa su ga mutanen da aka naɗa
su lura da aiki a kan haikalin UBANGIJI. Waɗannan mutane ne suke biyan ma'aikatan
da suka gyara suka kuma mai da haikalin. 11 Suka kuma ba da kuɗi ga kafintoci da
magina don su sayi sassaƙaƙƙun duwatsu, da katakai don yin tsaiko da tankar ginin
da sarakunan Yahuda suka bari yǎ fāɗi ya zama kango.
12 Mutanen fa suka yi aiki da aminci. Shugabanninsu, su ne Yahat da Obadiya,
Lawiyawa zuriyar Merari da Zakariya da Meshullam, zuriyar Kohat. Dukan
Lawiyawa waɗanda suke gwanaye a kayan kiɗi, 13 sun lura da ma'aikata, suka kuma
lura da dukan masu aiki daga aiki zuwa aiki. Waɗansu Lawiyawan su ne marubuta,
magatakarda da kuma masu tsaron ƙofofi.

*An sami Littafin Doka*
14 Yayinda suke fitar da kuɗin da aka kai cikin haikalin UBANGIJI, sai Hilkiya firist
ya sami Littafin Dokar UBANGIJI da aka bayar ta wurin Musa. 15 Hilkiya ya ce wa

Shafan magatakarda, “Na sami Littafin Doka a cikin haikalin UBANGIJI.” Sai ya ba wa Shafan.
16 Sa'an nan Shafan ya ɗauki littafin zuwa wurin sarki, ya faɗa masa, “Manyan
ma'aikatanka suna yin kome da aka sa su. 17 Mun ɗauke kuɗin da an ajiye a haikalin
UBANGIJI muka ba wa masu aiki da waɗanda suke lura da su.” 18 Sa'an nan Shafan
magatakarda ya sanar da sarki ya ce, “Hilkiya firist ya ba ni wani littafi.” Sai Shafan ya karanta daga cikinsa a gaban sarki.
19 Da sarki ya ji kalmomin Doka, sai ya yage rigunansa. 20 Ya ba da waɗannan
umarnai ga Hilkiya, Ahikam ɗan Shafan, Abdon ɗan Mika, Shafan magatakarda da
kuma Asahiya mai hidimar sarki. 21 Ya ce, “Ku tafi ku nemi nufin UBANGIJI saboda ni da kuma saboda raguwa a Isra'ila da Yahuda game da abin da aka rubuta a wannan littafin da aka samu. Fushin UBANGIJI mai girma ne da aka zuba a kanmu domin kakanninmu ba su kiyaye maganar UBANGIJI ba; ba su aikata bisa ga dukan abin da yake a rubuce a wannan littafi ba.”
22 Hilkiya tare da waɗanda sarki ya aika, suka tafi suka yi magana da annabiya Hulda, wadda take matar Shallum ɗan Tokhat ɗan Hasra, mai tsaron wurin ajiyar riguna. Tana zama a Urushalima, a Yanki na Biyu.
23 Sai ta ce musu, “Ga abin da UBANGIJI, Allah na Isra'ila ya ce faɗa wa mutumin
da ya aike ku gare ni, 24 ‘Ga abin da UBANGIJI ya ce zai kawo masifa a wannan wuri da mutanensa, dukan la'anar da aka rubuta a cikin littafin da aka karanta a gaban
sarkin Yahuda. 25 Domin sun yashe ni suka kuma ƙone turare wa waɗansu alloli, suka tsokane ni in yi fushi ta wurin dukan abin da hannuwansu suka yi, fushina zai
zuba a kan wannan wuri, ba kuma za a kwantar da shi ba.’ 26 Ku faɗa wa sarkin
Yahuda, wanda ya aike ku ku nemi nufin UBANGIJI, ‘Ga abin da UBANGIJI, Allah na
Isra'ila yake cewa game da kalmomin da ka ji. 27 Domin zuciyarka mai tuba ce, ka kuma ƙasƙantar da kanka a gaban Allah sa'ad da ka ji abin da ya yi magana a kan wannan wuri da mutanensa, domin kuma ka ƙasƙantar da kanka a gabana, ka yage
rigunanka ka kuma yi kuka a gabana, na ji ka, in ji UBANGIJI. 28 Yanzu zan tara ka da kakanninka, za a kuma binne ka cikin salama. Idanunka ba za su ga dukan masifar da zan kawo a kan wannan wuri da kuma a kan waɗanda suke zama a nan ba.’ ”

Sai suka kai amsar wa sarki.

*(2 Sarakuna 23.1-3)*

29 Sai sarki ya kira dukan dattawan Yahuda da Urushalima. 30 Ya haura zuwa
haikalin UBANGIJI tare da mutanen Yahuda, mutanen Urushalima, firistoci da Lawiyawa, dukan mutane daga ƙarami zuwa babba. Ya karanta dukan kalmomin
Littafin Alkawari wanda aka samu a cikin haikalin UBANGIJI a kunnuwansu. 31 Sai
sarkin ya miƙe tsaye a inda yake, ya sabunta alkawari a gaban UBANGIJI, don yǎ bi UBANGIJI yǎ kiyaye umarnansa, ƙa'idodinsa da kuma farillansa da dukan zuciyarsa da kuma dukan ransa, ya kuma yi biyayya da kalmomin alkawarin da aka rubuta a cikin wannan littafi.
32 Sa'an nan ya sa kowa a Urushalima da Benyamin ya yi alkawari ga wannan; mutanen Urushalima suka aikata wannan bisa ga alkawarin Allah, Allah na kakanninsu.
33 Yosiya ya fitar da dukan gumakan banƙyama daga dukan yankunan Isra'ilawa, ya kuma sa dukan waɗanda suke a Isra'ila su bauta wa UBANGIJI Allahnsu. Muddin ransa, ba su fasa bin UBANGIJI Allah na kakanninsu ba.

# 35

*Yosiya ya yi Bikin Ketarewa*
*(2 Sarakuna 23.21-23)*

1 Yosiya ya yi Bikin Ketarewa ga UBANGIJI a Urushalima, aka kuma yanka ɗan
ragon Bikin Ketarewa a ranar goma sha huɗu ga wata na farko. 2 Ya zaɓi firistoci su
yi aikinsu, sai ya ƙarfafa su su yi aikin da kyau a hidimar haikalin UBANGIJI. 3 Ya ce
wa Lawiyawa waɗanda suke koyar da dukan Isra'ila da kuma waɗanda aka tsarkake
wa UBANGIJI. "Ku sa akwatin alkawari mai tsarki a cikin haikalin da Solomon ɗan
Dawuda sarkin Isra'ila ya gina. Ba za a riƙa ɗaukansa a kafaɗa ba. Yanzu ku bauta
wa UBANGIJI Allahnku da kuma mutanensa Isra'ila. 4 Ku shirya kanku iyali-iyali a
sassanku, bisa ga umarnan da Dawuda sarkin Isra'ila da kuma ɗansa Solomon suka
rubuta.
5 "Ku tsaya a tsattsarkan wuri, bisa ga ƙungiyoyin gidajen kakannin 'yan'uwanku,
waɗanda su ba firistoci ba ne. Kowanne ya sami kashi daga cikin gidan Lawiyawa.
6 Ku yanka ragunan Bikin Ketarewa, ku tsarkake kanku, ku kuma shirya raguna
domin 'yan'uwanku, kuna yin abin da UBANGIJI ya umarta ta wurin Musa."
7 Yosiya ya tanada wa dukan mutanen da ba firistoci ba ne waɗanda suke a wurin,
tumaki da awaki dubu talatin don a yanka saboda hadayun Bikin Ketarewa, ya kuma
ba su shanu dubu uku. Dukan dabbobin kuwa daga garken sarki ne.
8 Fadawansa su ma suka ba da taimako da yardar rai ga mutane da kuma firistoci da
Lawiyawa. Hilkiya, Zakariya da Yehiyel masu aiki a haikalin Allah, suka ba firistoci
hadayun Bikin Ketarewa dubu biyu da ɗari shida da kuma shanu ɗari uku. 9 Haka
kuma Konaniya tare da Shemahiya da Netanel, ɗan'uwansa, da Hashabiya, Yehiyel
da Yozabad, shugabannin Lawiyawa, suka tanadar da hadayun Bikin Ketarewa dubu
biyar da kuma bijimai ɗari biyar domin Lawiyawa.
10 Sa'ad da aka shirya kome don Bikin Ketarewar, sai Firistoci tare da Lawiyawa
suka tsaya wurin tsayawarsu bisa ga umarnin sarki. 11 Aka yanka ragunan Bikin
Ketarewa, firistoci kuma suka yayyafa jinin da aka ba su, yayinda Lawiyawa suna
fiɗan dabbobi. 12 Suka keɓe hadayun ƙonawa don su ba da su ga ƙungiyoyin iyalan
mutane don su miƙa ga UBANGIJI, yadda yake a rubuce a Littafin Musa. Suka yi haka
da shanun. 13 Suka gasa dabbobin Bikin Ketarewa a bisa wuta yadda aka tsara, suka
dafa hadayu masu tsarki a tukwane, da manyan tukwane, da kuma kwanoni, suka
raba su nan da nan ga dukan mutane. 14 Bayan wannan, suka shirya wa kansu da
kuma wa firistoci, saboda firistoci, zuriyar Haruna, suna miƙa hadayun ƙonawa da
sashen kitse daga safe har dare. Saboda haka Lawiyawa suka shirya wa kansu da
kuma wa firistocin daga zuriyar Haruna.
15 Mawaƙa zuriyar Asaf, suna a wuraren da Dawuda, Asaf, Heman da Yedutun
mai duba na sarki suka tsara. Bai zama lalle matsaran ƙofofi a kowace ƙofa su bar
wuraren aikinsu ba, domin 'yan'uwansu Lawiyawa sun yi shiri dominsu.
16 Ta haka fa aka yi dukan hidimar UBANGIJI a wannan rana, domin su kiyaye Bikin
Ketarewa, domin kuma su miƙa hadayu na ƙonawa a bisa bagaden UBANGIJI, yadda
sarki Yosiya ya umarta. 17 Isra'ilawan da suka kasance a can suka yi Bikin Ketarewa
a wannan rana, suka kuma kiyaye Bikin Burodi Marar Yisti kwana bakwai. 18 Ba a
taɓa yin Bikin Ketarewa haka ba tun zamanin annabi Sama'ila; kuma babu sarkin
Isra'ilan da ya taɓa yin irin Bikin Ketarewa kamar yadda Yosiya ya yi, tare da firistoci,
Lawiyawa da kuma dukan Yahuda da Isra'ila, waɗanda suke can tare da mutanen
Urushalima. 19 An yi wannan Bikin Ketarewa a shekara ta goma sha takwas ta mulkin
Yosiya.

### *Mutuwar Yosiya*
### *(2 Sarakuna 23.28-30)*

20 Bayan wannan duka, sa'ad da Yosiya ya shirya haikali, Neko sarkin Masar ya
haura don yǎ yi yaƙi a Karkemish a Yuferites, sai Yosiya ya fita don yǎ fafata da shi a
yaƙi. 21 Amma Neko ya aiki 'yan saƙo ga Yosiya, yana cewa, "Me ya gama ni da kai,

ya Sarkin Yahuda? Ban zo in yi yaƙi da kai ba. Na zo ne in yi yaƙi da gidan da yake gāba da ni! Ka ƙyale ni! Allah ne ya riga ya faɗa mini in hanzarta. Kada ka yi gāba da Allah, wanda yake tare da ni, don kada yǎ hallaka ka.”
22 Yosiya fa, bai juya daga gare shi ba, amma ya ɓad da kama don yǎ yi yaƙin. Bai saurari abin da Neko ya faɗa bisa ga umarnin Allah ba, amma ya tafi ya yaƙe shi a filin Megiddo.
23 Maharba suka harbi Yosiya, sai ya ce wa hafsoshinsa, “Ku ɗauke ni ku fita da ni daga nan; gama an yi mini mummunan rauni.”
24 Saboda haka suka ɗauke shi a keken yaƙin, suka fitar da shi, suka sa shi a wata keken yaƙin da yake da shi, suka kawo shi Urushalima, inda ya mutu. Aka binne shi a makabartar kakanninsa, sai dukan Yahuda da Urushalima suka yi makoki dominsa.
25 Annabin Irmiya ya tsara waƙoƙin makoki domin Yosiya, wanda har wa yau mawaƙa maza da mata suke rera game da Yosiya. Suka sa waɗannan su zama al’ada a Isra’ila, suna kuma a rubuce cikin Littafin Makoki.
26 Sauran ayyukan mulkin Yosiya da kuma kyawawan abubuwan da ya yi, bisa ga abin da aka rubuta a Dokar Ubangiji,
27 dukan ayyukan, daga farko har zuwa ƙarshe, suna a rubuce cikin littafin sarakunan Isra’ila da na Yahuda.

# 36

1 Sai mutanen ƙasar suka ɗauki Yehoyahaz ɗan Yosiya suka naɗa shi sarki a Urushalima yǎ gāji mahaifinsa.

*Yehoyahaz sarkin Yahuda*
*(2 Sarakuna 23.31-34)*

2 Yehoyahaz yana da shekara ashirin da uku sa’ad da ya zama sarki, ya kuma yi mulki a Urushalima wata uku.
3 Sarkin Masar ya tumɓuke shi a Urushalima, ya tilasta Yahuda su biya haraji talenti ɗari na azurfa da kuma talentin zinariya.
4 Sarkin Masar ya naɗa Eliyakim, ɗan’uwan Yehoyahaz, sarki a bisa Yahuda da kuma Urushalima, ya kuma canja sunan Eliyakim zuwa Yehohiyakim. Amma Neko ya ɗauki Yehoyahaz ɗan’uwan Eliyakim ya kai Masar.

*Yehohiyakim sarkin Yahuda*
*(2 Sarakuna 23.36–24.7)*

5 Yehohiyakim yana da shekara ashirin da biyar sa’ad da ya zama sarki, ya kuma yi mulki a Urushalima shekara goma sha ɗaya. Ya yi abin da yake mugu a gaban Ubangiji Allahnsa.
6 Nebukadnezzar sarkin Babilon ya hauro ya kara da shi. Ya kama shi, ya daure da sarƙoƙin tagulla, ya kuma kai shi Babilon.
7 Nebukadnezzar sarkin Babilon ya kuma kwaso kayayyaki daga haikalin Ubangiji ya sa su a haikalinsa a can.
8 Sauran ayyukan mulkin Yehohiyakim, ayyukan banƙyamar da ya aikata da dukan abubuwan da aka same shi da su, suna a rubuce cikin littafin sarakunan Isra’ila da na Yahuda. Sai Yehohiyacin ɗansa ya gāje shi a matsayin sarki.

*Yehohiyacin sarkin Yahuda*
*(2 Sarakuna 24.8-17)*

9 Yehohiyacin yana da shekara goma sha takwas sa’ad da ya zama sarki, ya kuma yi mulki a Urushalima wata uku da kwana goma. Ya yi abin da yake mugu a gaban Ubangiji.
10 Da bazara, Sarki Nebukadnezzar ya aika a kawo Yehohiyacin, aka kuma kawo shi Babilon, tare da kayayyaki masu daraja daga haikalin Ubangiji, sai Sarki Nebukadnezzar ya naɗa kawunsa* Zedekiya, sarki a bisa Yahuda da Urushalima.

* **36:10** Da Ibraniyanci ɗan’uwa, wato, dangi (dubi 2Sar 24.17).

*Zedekiya sarkin Yahuda*
*(2 Sarakuna 24.18-20; Irmiya 52.1-3)*
11 Zedekiya yana da shekara ashirin da ɗaya sa'ad da ya zama sarki, ya kuma yi
mulki a Urushalima shekara goma sha ɗaya. 12 Ya yi abin da yake mugu a gaban
UBANGIJI Allahnsa kuma bai ƙasƙantar da kansa a gaban Irmiya annabi, wanda
ya yi magana kalmar UBANGIJI ba. 13 Ya tayar wa Sarki Nebukadnezzar, wanda
ya sa ya yi rantsuwa da sunan Allah. Ya zama mai kunnen ƙashi da kuma taurin
zuciya, bai kuwa juye ga UBANGIJI, Allah na Isra'ila ba. 14 Bugu da ƙari, dukan
shugabannin firistoci da mutane suka ƙara zama marasa aminci, suna bin dukan
abubuwan banƙyama na al'ummai, suka ƙazantar da haikalin UBANGIJI, wanda ya
tsarkake a Urushalima.

*Fāɗuwar Urushalima*
15 Sai UBANGIJI Allah na kakanninsu, ya yi ta aika da magana gare su ta wurin 'yan
saƙonsa sau da sau, domin ya ji tausayi mutanensa da mazauninsa. 16 Amma suka
yi wa 'yan saƙon Allah ba'a, suka rena maganarsa, suka yi wa annabawansa dariyar
reni, har sai da fushin UBANGIJI ya tasar a kan mutanensa babu makawa.
*(2 Sarakuna 25.1-21; Irmiya 52.3-30)*
17 Ya bashe su ga sarkin Babiloniyawa† wanda ya karkashe samarinsu da takobi a
wuri mai tsarki, bai yi juyayin saurayi, ko budurwa, ko tsoho, ko gajiyayye ba. Allah
ya bashe su duka ga Nebukadnezzar. 18 Nebukadnezzar ya kwashe dukan kayayyaki
daga haikalin Allah, babba da ƙarami, da ma'ajin haikalin UBANGIJI da kuma ma'ajin
sarki da na fadawansa zuwa Babilon. 19 Suka cinna wa haikalin Allah wuta, suka
rurrushe katangar Urushalima; suka ƙone dukan fada, suka kuma lalace kome mai
amfani da yake can.
20 Waɗanda ba a kashe ba kuwa Nebukadnezzar ya kwashe su, ya kai Babilon, suka
zama bayinsa da na 'ya'yansa maza har zuwa kahuwar mulkin Farisa. 21 Kasar ta
more hutun Asabbacinta; a dukan lokacin zamanta kango ta huta, har sai da shekaru
saba'in nan suka cika bisa ga maganar UBANGIJI da Irmiya ya faɗi.
*(Ezra 1.1-4)*
22 Don a cika maganar da UBANGIJI ya yi ta wurin Irmiya, a shekara farko ta Sairus
sarkin Farisa, sai UBANGIJI ya motsa zuciyar Sairus na Farisa don yǎ yi shela a dukan
masarautarsa, ya kuma sa shi a rubuce cewa,
23 "Ga abin da Sairus sarkin Farisa ya ce,
" 'UBANGIJI Allah na sama, ya ba ni dukan mulkokin duniya, ya kuma naɗa ni in
gina masa haikali a Urushalima a Yahuda. Duk wani na mutanensa a cikinku, bari
yǎ haura yǎ tafi, bari kuma UBANGIJI Allahnsa yǎ kasance tare da shi.' "

† **36:17** Ko kuwa Kaldiyawa

# Ezra

*Sairus ya taimaki Yahudawa su koma gida*

1 A shekara ta farko ta mulkin sarkin Farisa, wato, sarki Sairus, domin a cika
maganar UBANGIJI da aka yi ta bakin Irmiya, sai UBANGIJI ya taɓa zuciyar Sairus
sarkin Farisa ya yi shela a duk fāɗin ƙasarsa, ya kuma rubuta cewa,
2 "Ga abin da Sairus sarkin Farisa yake shela,
" 'UBANGIJI Allah na sama ya ba ni iko in yi mulkin duniya duka, ya kuma zaɓe ni
in gina masa haikali a Urushalima cikin Yahuda. 3 Duk wanda yake nasa a cikinku
bari Allahnsa yă kasance tare da shi, bari yă tafi Urushalima cikin Yahuda yă gina
haikalin UBANGIJI, Allah na Isra'ila, Allah wanda yake a Urushalima. 4 Duk inda
akwai mutumin Yahuda da ya rage, sai mutanen da suke zama kusa da shi, su
taimake shi da azurfa, da zinariya, da kaya, da kuma dabbobi, tare da kyautai na
yardar rai saboda Gidan Allah wanda yake a Urushalima.' "
5 Sai shugabannin zuriyar Yahuda da na Benyamin, da firistoci da Lawiyawa, duk
wanda Allah ya taɓa zuciyarsa, suka shirya don su je su gina haikalin UBANGIJI
a Urushalima. 6 Dukan maƙwabtansu kuwa suka taimake su da gudummawa na
kayan azurfa da na zinariya, da kaya, da dabbobi, da kuma kyautai masu daraja bisa
bayarwar yardar rai da suka yi.
7 Sai sarki Sairus ya fitar da kayan da suke na haikalin UBANGIJI waɗanda
Nebukadnezzar ya kwashe daga Urushalima ya sa a haikalin allahnsa.* 8 Sairus
sarkin Farisa ya sa Mitredat ma'aji ya ƙirga su a gaban Sheshbazzar ɗan sarkin
Yahuda.

9 Ga lissafin kayan.

| | |
|---|---|
| Manyan kwanonin zinariya guda | 30 |
| Manyan kwanonin azurfa guda | 1,000 |
| Wuƙaƙe guda | 29 |
| 10 Waɗansu kwanonin zinariya guda | 30 |
| Waɗansu kwanonin azurfa guda | 410 |
| da waɗansu kayayyaki guda | 1,000 |

11 Dukan kayayyakin zinariya da na azurfa sun kai 5,400.

Sheshbazzar ya kawo kayayyakin nan duka tare da shi lokacin da kamammun suka hauro daga Babilon zuwa Urushalima.

# 2

*Waɗanda suka dawo daga bauta*
*(Nehemiya 7.4-73)*

1 Ga lissafin waɗanda suka dawo daga bauta a Babilon, waɗanda Nebukadnezzar
sarkin Babilon ya kwasa zuwa bauta a ƙasar Babilon (sun dawo Urushal-
ima da Yahuda, kowa ya koma garinsu. 2 Sun komo tare da Zerubbabel, da

* **1:7** Ko kuwa alloli

Yeshuwa, da Nehemiya, da Serahiya, da Re'elaya, da Mordekai, da Bilshan,
da Misfar, da Bigwai, da Rehum, da Ba'ana).

Ga jerin mazan mutanen Isra'ila.
3 Zuriyar
Farosh mutum 2,172
4 ta Shefatiya 372
5 ta Ara 775
6 ta Fahat-Mowab (ta wurin Yeshuwa da Yowab) 2,812
7 ta Elam 1,254
8 ta Zattu 945
9 ta Zakkai 760
10 ta Bani 642
11 ta Bebai 623
12 ta Azgad 1,222
13 ta Adonikam 666
14 ta Bigwai 2,056
15 ta Adin 454
16 ta Ater (ta wurin Hezekiya) 98
17 ta Bezai 323
18 ta Yora 112
19 ta Hashum 223
20 ta Gibbar 95.
21 Mutanen
Betlehem 123
22 na Netofa 56
23 na Anatot 128
24 na Azmawet 42
25 na Kiriyat Yeyarim,* da Kefira Beyerot 743
26 na Rama da Geba 621
27 na Mikmash 122
28 na Betel da Ai 223
29 na Nebo 52
30 na Magbish 156
31 na ɗayan Elam ɗin 1,254
32 na Harim 320
33 na Lod, da Hadid da Ono 725
34 na Yeriko 345
35 na Sena'a 3,630.

36 Firistoci.
Zuriyar
Yedahiya (ta wurin iyalin Yeshuwa) 973
37 ta Immer 1,052
38 ta Fashhur 1,247
39 ta Harim 1,017.

40 Lawiyawa.
Lawiyawa na zuriyar
Yeshuwa da Kadmiyel (ta wurin Hodawiya) mutum 74.

41 Mawaƙa.
Zuriyar

* **2:25** Dubi Seftuwajin (dubi kuma Neh 7.29); da Ibraniyanci Kiriyat Arim

Asaf mutum 128.

42 Masu tsaron haikali.
Zuriyar
Shallum, Ater, Talmon,
Akkub, Hatita, da Shobai mutum 139.

43 Ma'aikatan haikali.
Zuriyar
Ziha, Hasufa, Tabbawot,
44 Keros, Siyaha, Fadon,
45 Lebana, Hagaba, Akkub,
46 Hagab, Shamlai, Hanan,
47 Giddel, Gahar, Reyahiya,
48 Rezin, Nekoda, Gazzam,
49 Uzza, Faseya, Besai,
50 Asna, Meyunawa, Nefussiyawa,
51 Bakbuk, Hakufa, Harhur,
52 Bazlut, Mehida, Harsha,
53 Barkos, Sisera, Tema,
54 Neziya da Hatifa.
55 Zuriyar bayin Solomon.
Zuriyar
Sotai, Hassoferet, Feruda,
56 Ya'ala, Darkon, Giddel,
57 Shefatiya, Hattil,
Fokeret-Hazzebayim, da Ami.
58 Dukan zuriyar ma'aikatan haikali, da kuma bayin Solomon 392.

59 Waɗannan mutanen ne suka zo daga garuruwan Tel-Mela, Tel-Harsha, Kerub, Addan da Immer, amma ba su iya nuna ainihin tushensu daga Isra'ila ba.
60 'Yan zuriyar
Delahiya, Tobiya, da Nekoda 652.

61 Daga cikin firistoci kuma,
zuriyar
Hobahiya, Hakkoz da Barzillai (wanda ya auri diyar Barzillai mutumin Gileyad da ake kuma kira da wannan suna).
62 Waɗannan sun nemi sunayen iyalansu a cikin littafin da ake rubuta sunayen amma ba su ga sunayensu ba, saboda haka sai aka hana su zama firistoci domin an ɗauka su marasa tsabta ne. 63 Gwamna ya umarce su cewa kada su ci wani abinci mai tsarki sai firist ya yi shawara ta wurin Urim da Tummim tukuna.

64 Yawan jama'ar duka ya kai mutum 42,360, 65 ban da bayinsu maza da mata 7,337; suna kuma da mawaƙa maza da mata 200. 66 Suna da dawakai guda 736, alfadarai 245, 67 raƙuma 435, da jakuna 6,720.

68 Sa'ad da suka isa haikalin UBANGIJI a Urushalima, sai waɗansu shugabannin iyalai suka yi bayarwar yardar rai ta gudummawarsu domin sāke gina gidan Allah a wurin

da yake. 69 Bisa ga ƙarfinsu suka bayar da darik 61,000 na zinariya, da maina 5,000
na azurfa, da rigunan firistoci guda 100.
70 Firistoci, da Lawiyawa, da mawaƙa, da masu tsaron ƙofofi, da masu aiki a haikali,
tare da waɗansu mutane, da dukan sauran Isra'ilawa suka zauna a garuruwansu.

# 3

*Sāke gina bagadi*

1 Da tsayawar watan bakwai, sai Isra'ilawa waɗanda suka koma garuruwansu suka
taru da nufi ɗaya a Urushalima. 2 Sai Yeshuwa ɗan Yozadak da sauran firistoci,
da Zerubbabel ɗan Sheyaltiyel da abokan aikinsa, suka fara gina bagaden Allah na
Isra'ila don miƙa hadaya ta ƙonawa bisa ga abin da yake a rubuce a Dokar Musa
mutumin Allah. 3 Duk da tsoron da suke ji na mutanen da suke kewaye da su, sun gina
bagaden a wurinsa, suka kuma miƙa hadaya ta ƙonawa a kan bagaden ga Ubangiji
safe da yamma. 4 Bisa ga abin da yake a rubuce kuma, suka yi biki Bikin Tabanakul,
suka miƙa hadayu kowace rana gwargwadon yawan hadayun da ake bukata. 5 Bayan
wannan, suka miƙa hadayu na ƙonawa yadda aka saba. Suka miƙa hadayu na Sabon
Wata, da hadayu na bukukkuwan Ubangiji, da kuma hadayun da aka bayar da yardar
rai ga Ubangiji. 6 A ranar farko ta watan bakwai, sai suka fara miƙa hadaya ta ƙonawa
ga Ubangiji, ko da yake ba a riga an aza harsashin ginin haikalin Ubangiji ba.

*Sāke gina haikali*

7 Sai suka ba wa magina da kafintoci kuɗi, suka ba wa mutanen Sidon da na Taya
abinci, da abin sha, da mai, don su kawo itatuwan al'ul a Yaffa daga Lebanon ta teku,
yadda Sairus sarkin Farisa ya ba da umarni.
8 A wata na biyu na shekara ta biyu, bayan sun komo gidan Allah a Urushalima, sai
Zerubbabel ɗan Sheyaltiyel, Yoshuwa ɗan Yozadak da sauran 'yan'uwansa (Firistoci
da Lawiyawa da duk waɗanda suka komo Urushalima daga bauta) suka fara aiki,
aka zaɓi Lawiyawa daga masu shekaru ashirin da haihuwa zuwa waɗanda suka
wuce haka don su dubi aikin ginin gidan Ubangiji. 9 Yeshuwa da 'ya'yansa maza, da
'yan'uwansa, da Kadmiyel da 'ya'yan Yahuda ('yan zuriyar Hodawiya), da 'ya'yan
Henadad, da 'ya'yansu da 'yan'uwansu, dukansu Lawiyawa ne, suka haɗa kai cikin
duban masu aikin gidan Allah.
10 Da masu ginin suka aza harsashin ginin haikalin Ubangiji, sai firistoci suka sa
kayansu na firistoci suka riƙe ƙahonin busa, Lawiyawa ('ya'yan Asaf) kuwa suka
riƙe kuge, suka yi shiri domin su rera yabo ga Ubangiji kamar yadda Dawuda Sarkin
Isra'ila ya ba da umarni. 11 Suka rera waƙar yabo da godiya ga Ubangiji, suna cewa,
"Shi nagari ne;
ƙaunarsa kuwa ga Isra'ila har abada ce."
Dukan jama'a kuwa suka yabi Ubangiji da murya mai ƙarfi, domin an aza harsashin
ginin gidan Ubangiji. 12 Amma tsofaffin firistoci, da Lawiyawa, da shugabannin iyalai
da yawa, waɗanda dā suka ga yadda haikali na farko yake, suka fashe da kuka mai
ƙarfi sa'ad da suka ga an aza harsashin ginin wannan haikali, yayinda waɗansu
kuma suka yi ihu da farin ciki. 13 Ba wanda zai iya rabe tsakanin ihun farin ciki da
na kuka, domin mutanen sun tā da murya sosai har aka ji su daga nesa.

# 4

*Hamayya da sāke ginin*

1 Sa'ad da abokan gāban Yahuda da na Benyamin suka ji cewa waɗanda suka
dawo daga bauta suna gina haikalin Ubangiji, Allah na Isra'ila 2 sai suka zo wurin
Zerubbabel da kuma wurin shugabannin iyalai, suka ce, "Bari mu taimake ku ginin

domin mu ma muna addu'a ga Allahnku yadda kuke yi, muna miƙa masa hadaya tun lokacin Esar-Haddon sarkin Assuriya wanda ya kawo mu nan."

3 Amma Zerubbabel, Yeshuwa, da sauran shugabannin iyalai na Isra'ila suka amsa suka ce, "Ba za ku sa hannu cikin gina wa Allahnmu haikali ba, mu kaɗai za mu gina wa UBANGIJI, Allah na Isra'ila gini kamar yadda Sarki Sairus, sarkin Farisa, ya umarce mu."

4 Sai mutanen da suke zama a wurin suka fara yin ƙoƙari su sa mutanen Yahuda su
karaya, suka sa su ji tsoron ci gaba da ginin. 5 Suka yi hayar mashawarta don su
ga cewa sun ɓata ƙoƙarinsu dukan kwanakin mulkin Sairus sarkin Farisa har zuwa kwanakin mulkin Dariyus sarkin Farisa.

## *Hamayya na baya a ƙarƙashin Zerzes da Artazerzes*

6 A farkon mulkin Zerzes, sai abokan gāba suka kawo ƙarar mutanen Yahuda da na Urushalima.

7 A zamanin Artazerzes sarkin Farisa kuma, sai Bishlam, da Mitredat, da Tabeyel, da sauran abokansu suka rubuta wasiƙa zuwa ga Artazerzes. Aka rubuta wasiƙar da harufan Arameyik, aka kuma fassara ta a yaren Arameyik.

8 Rehum shugaban rundunar soja, da Shimshai marubuci, suka rubuta wasiƙar a kan Urushalima zuwa ga sarki Artazerzes, suka ce.

9 Rehum shugaban sojoji, da Shimshai marubuci, da sauran abokansu, wato, alƙalai, da masu riƙe da muƙamai daga Farisa, Uruk da Babilon, mutanen Elam da na
Shusha, 10 da sauran mutane waɗanda mai girma Osnaffar ya kwaso, ya zaunar da su cikin birnin Samariya da sauran wurare na Kewayen Kogin Yuferites.

11 (Ga abin da suka rubuta.)

Zuwa ga sarki Artazerzes.

Daga bayinka, mutanen Kewayen Kogin Yuferites.

12 Ya kamata sarki ya san cewa Yahudawan da suka hauro wurinmu daga wurinka, sun je Urushalima suna sāke gina wannan mugun birni mai tawaye. Suna sāke gyara katangar, suna kuma gyara harsashin katangar.

13 Ya kamata fa, sarki ya san cewa in aka sāke gina wannan birni duk da katangar birnin, mutanen birnin ba za su dinga biyan haraji, da kuɗin shiga, da na fitar
da kaya ba, wannan zai sa aljihun masarauta yǎ bushe. 14 Tun da yake muna
ƙarƙashin fada, bai kyautu mu bari a rena sarki ba, Saboda haka muke sanar da
sarki, 15 domin a bincika a littattafan tarihin kakanninka. Za ka ga cewa wannan birni mai tawaye ne. Tun daga zamanin dā wannan birnin yana ba sarakuna da
yankuna damuwa. Wannan ne ya sa aka ragargazar da birnin. 16 Muna sanar da
sarki cewa in har aka sāke gina wannan birnin da katangarsa, zai zama ka rasa kome a gefen Kewayen Kogin Yuferites ke nan.

17 Sarki ya aika da wannan amsa.

Zuwa ga Rehum shugaban sojoji, Shimshai marubuci da kuma sauran abokansu waɗanda suke zama a Samariya da kuma sauran wurare a Kewayen Kogin Yuferites.

Gaisuwa.

18 An karanta, an kuma fassara mini wasiƙar da kuma aika. 19 Na ba da umarni
aka kuma yi bincike, aka tarar cewa wannan birni ya daɗe yana yi wa sarakuna
tawaye, an yi tashin hankali a birnin. 20 Urushalima ta yi sarakuna masu iko sosai
waɗanda suka yi mulkin Kewayen Kogin Yuferites gaba ɗaya, an kuma biya masu
haraji, da kuɗin shiga da na fita na kaya. 21 Saboda haka sai ku ba da umarni yanzu
cewa mutanen su daina wannan aiki sai lokacin da na ba da umarni. 22 Ku tabbata
ka ɗauki wannan da muhimmanci. Don me za a bari wannan abu yǎ zama abin damuwa ga sarauta?

23 Da gama karanta wasiƙar sarki Artazerzes wa Rehum da Shimshai marubuci, da
abokansu, sai suka yi sauri suka je wurin Yahudawa a Urushalima, suka hana su
aikin ƙarfi da yaji.

24 Saboda haka aikin a gidan Allah a Urushalima ya tsaya cik sai a shekara ta biyu ta
mulkin Dariyus sarkin Farisa.

# 5

## *Wasiƙar Tattenai zuwa ga Dariyus*

1 Sai annabi Haggai, da annabi Zakariya zuriyar Iddo, suka yi wa Yahudawa a Yahuda
da Urushalima annabci a cikin sunan Allah na Isra'ila wanda yake da mulki a kansu.
2 Sa'an nan Zerubbabel ɗan Sheyaltiyel da Yeshuwa ɗan Yozadak suka yi shiri suka
kama aikin sāke gina gidan Allah a Urushalima. Annabawan Allah kuwa suna tare
da su, suna taimakonsu.

3 A wannan lokaci, Tattenai gwamnan Kewayen Kogin Yuferites, da Shetar-Bozenai
da abokansu suka je wurinsu suka tambaye su cewa, "Wa ya ba ku iko ku sāke
gina wannan haikali har ku gyara katangar?" 4 Suka kuma tambaye su "Ina sunayen
waɗanda suke wannan gini?" 5 Amma Allah yana tsaron dattawan Yahudawa, saboda
haka ba a hana su aikin ba har sai rahoto ya kai wurin Dariyus aka kuma sami
amsarsa a rubuce tukuna.

6 Ga wasiƙar da Tattenai, gwamnan Kewayen Kogin Yuferites, da Shetar-Bozenai da
abokansu masu riƙe da muƙamai a Kewayen Kogin Yuferites suka aika wa Sarki
Dariyus. 7 Ga rahoton da suka aika masa.

Zuwa ga Sarki Dariyus.

Gaisuwa da fatan alheri.

8 Ya kamata sarki yǎ sani cewa mun je yankin Yahuda, zuwa gidan Allah mai girma.
Muka ga mutanen suna ginin haikalin da manyan duwatsu, suna sa katakai a
bangon. Ana aikin da ƙwazo, aikin kuma yana cin gaba sosai, suna kuma lura
da shi.

9 Mun tambayi dattawan muka ce musu, "Wa ya ba ku iko ku sāke gina wannan
haikali, ku kuma sāke gyara katangarsa?" 10 Muka kuma tambaye su sunayensu
don mu rubuta mu sanar da kai waɗanda suke shugabanninsu.

11 Wannan ita ce amsar da suka ba mu.

"Mu bayin Allah na sama da ƙasa ne, muna sāke gina haikalin da aka gina tun
shekaru da yawa da suka wuce, da wani babban sarkin Isra'ila ya gina ya kuma
gama. 12 Amma domin kakanninmu sun ɓata wa Allah na sama rai, sai ya bari
suka fāɗa cikin hannun Nebukadnezzar mutumin Kaldiya, sarkin Babilon, wanda
ya rushe wannan haikali, ya kuma kwashe mutane zuwa Babilon.

13 "Duk da haka, a shekara ta farko ta mulkin Sairus sarkin Babilon, Sarki Sairus ya
ba da umarni cewa a sāke gina wannan gidan Allah. 14 Ya kuma kwashe kwanonin
zinariya da azurfa na gidan Allah daga haikalin Babilon waɗanda Nebukadnezzar
ya kwasa daga haikali a Urushalima. Sa'an nan sarki Sairus ya ba wa wani mutum
mai suna Sheshbazzar umarni wanda ya sa ya zama gwamna, 15 ya ce masa, 'Ka
kwashe kayan nan ka je ka zuba su a cikin haikalin Allah a Urushalima. Ka kuma
sāke gina gidan Allah a wurin da yake a dā.'

16 "Saboda haka Sheshbazzar ya so ya aza harsashin gina gidan Allah a Urushalima.
Tun daga wancan lokaci har zuwa yau ana kan gina shi amma ba a gama ba."

17 Yanzu in sarki yana so, bari a duba cikin littattafan tarihi na sarakuna na Babilon a gani ko lalle sarki Sairus ya ba da umarni a sāke gina gidan Allah a Urushalima. Bari sarki yă aiko mana da abin da ya gani game da wannan abu.

# 6

*Umarnin Dariyus*

1 Sarki Dariyus kuwa ya ba da umarni a bincika a duba cikin littattafan tarihin da
suke a ajiye a wurin ajiyarsu a Babilon. 2 Sai aka sami takarda a Ekbatana a yankin
Mediya, ga kuma abin da yake rubuce a ciki.

Abin tunawa.

3 A shekara ta farko ta mulkin sarki Sairus, sarki ya ba da umarni game da haikalin Allah a Urushalima, ya ce,

Bari a sāke gina haikalin yă zama wurin miƙa hadayu, a kuma aza harsashin ginin
haikalin. Tsayinsa zai zama ƙafa tasaʼin, fāɗinsa kuma kamu tasaʼin. 4 Za a jera
manyan duwatsu jeri uku, da jeri ɗaya na katako. Daga asusun sarki kuma za
a biya kuɗin aikin. 5 Kwanonin zinariya da na azurfan gidan Allah waɗanda
Nebukadnezzar ya kwashe daga haikali a Urushalima ya kawo Babilon, a mayar
da su wurinsu a haikali a Urushalima; a sa su cikin gidan Allah.

6 Saboda haka Tattenai, gwamnan Kewayen Kogin Yuferites, da Shetar-Bozenai, da ku
masu muƙami na yankin, ku bar wurin. 7 Kada ku hana wannan aiki na haikalin
Allah. Bari gwamnan Yahudawa, da dattawan Yahudawa su sāke gina wannan
gidan Allah a wurin da yake a dā.

8 Na kuma ba da umarni game da abin da za ku yi wa dattawan Yahudawa cikin aikin ginin wannan gidan Allah.

Daga asusun sarki a kuɗin da yake shigo wa Kewayen Kogin Yuferites za a biya
mutanen nan duka, domin kada aikin yă tsaya. 9 A tanada musu duk abin da suke
bukata. A ba su ʼyan bijimai, da raguna, da ʼyan tumaki domin miƙa hadaya ta
ƙonawa ga Allah na sama, haka kuma dole a tanada wa firistoci alkama, da gishiri,
da ruwan inabi, da mai, kullum ba fasawa yadda firistoci suke yi a Urushalima
10 domin su miƙa hadayu masu daɗi ga Allah na Sama, su kuma yi adduʼa domin
lafiyar sarki da ʼyaʼyansa.

11 Na kuma yi umarni cewa duk wanda ya karya wannan doka sai a fitar da itace
daga cikin gidansa, a fiƙe kan itacen, a tsire mutumin, saʼan nan a mai da gidansa
juji. 12 Bari Allah yă sa sunansa yă kasance, yă hamɓarar da duka wani sarki
ko mutanen da za su sa hannu don a sāke wannan doka, ko kuma don su rushe
haikalin nan a Urushalima.

Ni Dariyus na ba da wannan umarni, bari a yi biyayya babu wasa.

*Gamawa da kuma keɓewar haikali*

13 Saboda umarnin da sarki Dariyus ya aika, sai Tattenai, gwamnan Kewayen Kogin
Yuferites da Shetar-Bozenai da abokansu suka yi biyayya da umarnin babu wasa.
14 Dattawan Yahuda kuwa suka ci gaba da ginin suna yin nasara ta wurin waʼazin
Haggai annabi da Zakariya ɗan Iddo. Suka kuma gama ginin haikalin bisa ga
umarnin Allah na Israʼila da kuma umarnin Sairus da Artazerzes, sarakunan Farisa.
15 An gama ginin haikalin a rana ta uku na watan Adar a shekara ta shida ta mulkin
Sarki Dariyus.
16 Sai mutanen Israʼila, firistoci, Lawiyawa da kuma sauran waɗanda suka dawo daga
bauta suka yi bikin keɓe gidan Allah, cike da farin ciki. 17 Suka miƙa bijimai guda
ɗari, da raguna ɗari biyu, da ʼyan raguna ɗari huɗu. Suka kuma miƙa hadayu don

zunubi saboda dukan Isra'ila, suka kuma miƙa bunsurai guda goma sha biyu don
hadaya ta zunubi, kowane bunsuru ɗaya don kowace kabila ta Isra'ila. 18 Suka kuma
naɗa firistoci a gundumominsu da kuma Lawiyawa a ƙungiyoyinsu don hidimar
Allah a Urushalima, bisa ga abin da aka rubuta a Littafin Musa.

*Bikin Ketarewa*

19 A rana ta goma sha huɗu ga watan farko, sai waɗanda suka dawo daga bauta
suka yi Bikin Ketarewa. 20 Firistoci da Lawiyawa suka tsarkake kansu, suka zama
da tsabta. Lawiyawa suka yanka ragon Bikin Ketarewa domin dukan waɗanda suka
dawo daga bauta, da kuma domin 'yan'uwansu firistoci, da kuma domin kansu. 21 Sai
Isra'ilawa waɗanda suka dawo daga bauta suka ci tare da duk waɗanda suka keɓe
kansu daga halin ƙazanta na Al'ummai maƙwabtansu, don su nemi UBANGIJI, Allah
na Isra'ila. 22 Suka yi kwana bakwai suna Bikin Burodi Marar Yisti, suna cike da
farin ciki, gama UBANGIJI ya cika su da farin ciki don ya sa sarkin Assuriya ya canja
tunaninsa, ya taimake su cikin aikin gidan Allah, Allah na Isra'ila.

# 7

*Ezra ya zo Urushalima*

1 Bayan waɗannan abubuwa, a zamanin Artazerzes sarkin Farisa, sai Ezra ɗan
Serahiya, ɗan Azariya, ɗan Hilkiya, 2 ɗan Shallum, ɗan Zadok, ɗan Ahitub, 3 ɗan
Amariya, ɗan Azariya, ɗan Merahiyot, 4 ɗan Zerahiya, ɗan Uzzi, ɗan Bukki, 5 ɗan
Abishuwa, ɗan Finehas, ɗan Eleyazar, ɗan Haruna babban firist. 6 Shi Ezra ɗin ya zo
daga Babilon. Shi malami ne ya kuma san Dokar Musa sosai wadda UBANGIJI, Allah
na Isra'ila ya bayar. Sarki ya ba shi duk abin da ya roƙa, gama UBANGIJI Allahnsa
yana tare da shi. 7 Waɗansu Isra'ilawa, haɗe da firistoci, da Lawiyawa, da mawaƙa,
da masu tsaron ƙofofi, da masu aiki a haikali su ma suka zo Urushalima a shekara
ta bakwai a zamanin mulkin sarki Artazerzes.
8 Ezra ya iso Urushalima a wata na biyar na shekara ta bakwai na kama mulkin
sarkin. 9 Ya fara tafiyarsa daga Babilon a rana ta farko ga watan farko, ya kuma iso
Urushalima a rana ta farko ga watan biyar, gama alherin Allahnsa yana tare da shi.
10 Gama Ezra ya miƙa kansa ga bincike da kuma kiyaye Dokar UBANGIJI, da kuma
koya wa Isra'ilawa dokoki da kuma umarnan UBANGIJI.

*Wasiƙar sarki Artazerzes zuwa ga Ezra*

11 Ga wasiƙar da sarki Artazerzes ya ba Ezra wanda yake firist da kuma malami,
mutumin da yake cike da sani game da dokoki da kuma umarnan UBANGIJI wa Isra'ila.
12 Artazerzes, sarkin sarakuna.
Zuwa ga Ezra firist, malamin Dokar Allah na sama.
Gaisuwa.
13 Yanzu ina ba da umarni cewa duk wani mutumin Isra'ilan da yake cikin mulkina,
haɗe da firistoci, da Lawiyawa, da suke so su tafi tare da kai zuwa Urushalima
za su iya tafiya. 14 Sarki ne da mashawartansa guda bakwai suka aike ka don
ka je ka ga halin da Yahuda da Urushalima suke ciki game da dokokin Allahnka,
waɗanda suke a hannunka. 15 Za ka kuma tafi da zinariya da azurfa waɗanda
sarki da mashawartansa suka ba da kyautar yardar rai ga Allah na Isra'ila, wanda
haikalinsa ke a Urushalima, 16 haɗe da duk zinariya da azurfan da za ka iya samu a
Babilon, da kuma duk bayarwar yardar rai daga mutane da firistoci, domin haikalin
Allahnsu da yake a Urushalima. 17 Ka tabbata ka yi amfani da kuɗin nan don ka
sayi bijimai, da raguna, da 'yan raguna, da hadayu na gari, da na sha, ka kuma
miƙa su a kan bagade na haikalin Allahnka a Urushalima.

18 Sa'an nan kai da 'yan'uwanka Yahudawa ku yi abin da kuka ga ya fi kyau da sauran
zinariya da azurfa ɗin bisa ga nufin Allah. 19 Ka kai wa Allah na Urushalima duk
kayan da aka ba ka amanarsu don yin sujada a haikalin Allahnka. 20 Duk kuma
wani abin da ake bukata domin haikalin Allahnka, daga ɗakunan ajiya sarki za ka
fitar da kuɗin.
21 Yanzu fa ni, Sarki Artazerzes, ina ba da umarni ga kowane ma'aji na Kewayen Kogin
Yuferites su tanada duk abin da Ezra firist, wanda kuma yake malamin Dokar Allah
na sama zai bukaci, 22 har zuwa talenti ɗari na azurfa, da mudu ɗari na alkama,
da garwa ɗari na ruwan inabi, da garwa ɗari na man zaitun, da kuma gishiri ba
iyaka. 23 A yi duk abin da Allah na sama ya ce don haikalin Allah na sama, sai a yi
shi da himma. Me zai sa a jawo wa sarki da 'ya'yansa fushin Allah? 24 Ku kuma san
cewa, ba ku da ikon sa firistoci, da Lawiyawa, da mawaƙa, da masu tsaron ƙofofin
haikali, da masu aiki a gidan Allah, ko waɗansu masu aiki a haikali su biya haraji,
ko kuɗin shiga.
25 Kai kuma Ezra, bisa ga hikimar da Allah ya ba ka, sai ka zaɓi mahukunta da
alƙalai waɗanda za su zama masu yanke hukunci ga dukan mutanen Kewayen
Kogin Yuferites, duk waɗanda suka san dokokin Allahnka, ka kuma koya wa duk
waɗanda ba su san dokokin ba. 26 Ba shakka duk wanda bai yi biyayya da dokokin
Allahnka ba, da kuma dokokin sarki ba dole a yanke masa hukuncin kisa, ko
hukuncin kora, ko hukuncin raba shi da mallakarsa, ko kuma hukuncin kulle shi a
kurkuku.
27 Yabo ya tabbata ga Ubangiji Allah na kakanninmu, ya taɓa zuciyar sarki don yă
kawo ɗaukaka ga haikalin Allah a Urushalima ta wannan hanya. 28 Wanda kuma ya
sa na sami tagomashi a gaban sarki da mashawartansa, da kuma duk manyan masu
muƙami nasa. Gama Ubangiji Allahna yana tare da ni, sai na sami ƙarfin hali na
tattara shugabannin mutane daga Isra'ila, don mu tafi tare.

# 8

*Jerin shugabannin iyalan da suka dawo tare da Ezra*

1 Waɗannan su ne shugabannin iyalai, da kuma waɗanda suka dawo tare da ni daga
Babilon a zamanin mulkin Sarki Artazerzes.

2 Daga zuriyar Finehas,
Gershom ne shugaba;
daga zuriyar Itamar,
Daniyel ne shugaba;
daga zuriyar Dawuda,
Hattush 3 ɗan zuriyar Shekaniya ne shugaba,
daga zuriyar Farosh,
Zakariya ne shugaba, tare da shi akwai mutum 150;
4 daga Fahat-Mowab,
Eliyehoyenai ɗan Zerahiya ne shugaba, tare da shi akwai mutum 200;
5 daga zuriyar Zattu,
Shekaniya ɗan Yahaziyel ne shugaba, tare da shi akwai mutum 300;
6 daga zuriyar Adin,
Ebed ɗan Yonatan ne shugaba, tare da shi akwai mutum 50;
7 daga zuriyar Elam,
Yeshahiya ɗan Ataliya ne shugaba, tare da shi akwai mutum 70;
8 daga zuriyar Shefatiya,
Zebadiya ɗan Mika'ilu ne shugaba, tare da shi akwai mutum 80;

9 daga iyalin Yowab,
Obadiya ɗan Yehiyel ne shugaba, tare da shi akwai mutum 218;
10 daga Bani,
Shelomit ɗan Yosifiya ne shugaba, tare da shi akwai mutum 160;
11 daga Bebai,
Zakariya ɗan Bebai ne shugaba, tare da shi akwai mutum 28;
12 daga iyalin Azgad,
Yohanan ɗan Hakkatan ne shugaba, tare da shi akwai mutum 110;
13 zuriya ta Adonikam ne suka zo daga ƙarshe,
sunayensu kuwa su ne Elifelet, Yehiyel da Shemahiya, tare da su akwai mutum 60;
14 daga zuriyar Bigwai,
Uttai da Zakkur ne shugabanni, tare da su akwai mutum 70.

*Dawowa Urushalima*
15 Na kuma tattara su a bakin rafi wanda yake gangarawa zuwa Ahawa, muka kafa
sansani a can kwana uku. Da na bincika cikin mutane da firistoci, sai na tarar babu
Lawiyawa. 16 Saboda haka sai na aika a kira Eliyezer, da Ariyel, da Shemahiya, da
Elnatan, da Yarib, da Natan, da Zakariya, da Meshullam waɗanda su ne shugabanni.
Na kuma sa a kira Yohiyarib da Elnatan waɗanda masana ne. 17 Na sa su je wurin
Iddo wanda yake shugaba a Kasifiya. Aka gaya musu abin da za su gaya wa Iddo da
'yan'uwansa masu aiki a haikali a Kasifiya don su aiko mana waɗanda za su yi mana
hidima a haikalin Allahnmu. 18 Da yake Allah yana tare da mu, sai suka aiko mana da
Sherebiya, wanda ya iya aiki, shi daga zuriyar Mali ɗan Lawi ne, ɗan Isra'ila. Sai ya
zo tare da 'ya'yansa da kuma 'yan'uwansa. Dukansu dai mutum 18 ne. 19 Suka kuma
aika da Hashabiya tare da Yeshahiya daga zuriyar Merari, da 'yan'uwansu da kuma
'ya'yansu, su kuma mutum 20 ne. 20 Sun kuma kawo masu aiki a haikali mutum 220,
ƙungiyar da Dawuda da abokan aikinsa suka keɓe don su taimaki Lawiyawa aiki.
Duk aka rubuta waɗannan da sunayensu.
21 A can, a bakin rafin Ahawa, na sa mu yi azumi, domin mu ƙasƙantar da kanmu
a gaban Allah, mu kuma roƙe shi yǎ kiyaye mana hanya, da mu da 'ya'yanmu da
kayanmu duka. 22 Na ji kunya in roƙi sarki yǎ haɗa mu da sojoji da masu dawakai
don su yi mana rakiya su kāre mu daga magabta a kan hanya, gama mun ce wa sarki,
"Alherin Allah yana tare da duk wanda yake dogara gare shi, amma kuma fushinsa
yana kan duk wanda ya juya masa baya." 23 Saboda haka sai muka yi azumi, muka
kai roƙonmu a wurin Allah, ya kuwa amsa mana.
24 Sai na keɓe manyan firistoci guda goma sha biyu tare da Sherebiya, Hashabiya
da kuma 'yan'uwansu guda goma. 25 Na auna musu zinariya da azurfa, da kwanoni
waɗanda sarki da mashawartansa, da sauran abokan aikinsa, da Isra'ilawan da suke
can suka bayar domin haikalin Allahnmu. 26 Na auna musu talenti 650 na azurfa,
talenti ɗari na kwanonin azurfa, talenti 100 na zinariya, 27 kwanonin zinariya guda
20 da darajarsu ya kai darik 1,000, da kwanoni biyu na gogaggen tagulla, wanda yake
darajarsa daidai da zinariya.
28 Na ce masa, "Ku da kayan nan tsarkaka ne ga UBANGIJI. Azurfa da zinariya ɗin,
bayarwa ce ta yardar rai ga UBANGIJI, Allah na kakanninku. 29 Ku lura da su da kyau
har sai kun isa Urushalima. Ku auna su a shirayin haikalin UBANGIJI a Urushalima, a
gaban manyan firistoci, da Lawiyawa, da shugabannin iyalai na Isra'ila." 30 Sa'an nan
sai firistoci, da Lawiyawa suka karɓi azurfa da zinariya da kuma tsarkakan kwanonin
da aka auna don a kai haikalin Allahnmu a Urushalima.
31 A rana ta goma sha biyu ga watan farko, muka tashi daga bakin rafin Ahawa don
mu tafi Urushalima. Alherin Allahnmu yana tare da mu, ya kuma kāre mu daga
magabta da 'yan fashi. 32 Muka iso Urushalima, inda muka huta kwana uku.

33 A rana ta huɗu muka tafi haikalin Allah, muka auna azurfa, da zinariya, da
tsarkakan kwanonin, muka ba Meremot ɗan Uriya firist, da Eleyazar ɗan Finehas
yana tare da shi, da kuma Lawiyawan nan, wato, Yozabad ɗan Yeshuwa, da Nowadiya
ɗan Binnuyi. 34 Aka yi lissafi aka auna kome aka tarar yana nan daidai, aka kuma
rubuta yawan nauyin a lokacin.
35 Sa'an nan sai waɗanda suka dawo daga bauta suka miƙa hadaya ta ƙonawa ga
Allah na Isra'ila. Wato, bijimai guda goma sha biyu don Isra'ilawa duka, raguna
tasa'in da shida, 'yan raguna saba'in da bakwai, bunsurai kuma guda goma sha biyu.
Aka miƙa su hadaya don zunubi. Wannan duka hadaya ta ƙonawa ce ga UBANGIJI.
36 Suka kuma kai saƙon sarki zuwa ga wakilansa, da kuma gwamnoni na Kewayen
Kogin Yuferites waɗanda suka taimaki mutane da kuma gidan Allah.

# 9

*Addu'ar Ezra game da auratayya*

1 Bayan an yi waɗannan abubuwa duka, sai shugabanni suka zo wurina suka ce,
"Mutanen Isra'ila, har da firistoci da Lawiyawa ba su keɓe kansu daga maƙwabtansu
ba, ba su kuma keɓe kansu daga irin rayuwar ƙazantar mutanen ƙasar ba, wato,
rayuwar irinta Kan'aniyawa, da Hittiyawa, da Ferizziyawa, da Yebusiyawa, da
Ammonawa, da Mowabawa, da Masarawa da Amoriyawa. 2 Sun auro wa kansu da
'ya'yansu 'yan mata mutanen nan, ta haka aka kwaɓa zuriyar da aka tsarkake da ta
mutanen nan da suke tare da su. Shugabanni da manyan ma'aikata su ne a gaba-gaba
a aikata wannan abin kunya."
3 Sa'ad da na ji wannan, sai na yaga rigata da alkyabbata, na tsittsige gashin kaina da
na gemuna, na zauna, na rasa abin da yake mini daɗi. 4 Sai duk waɗanda suke tsoron
maganar Allah na Isra'ila suka kewaye ni don su ji wannan rashin imani wanda
waɗanda suka dawo bauta suka yi. Na kuwa zauna a can a rikice, har lokacin miƙa
hadaya na yamma.
5 Sa'an nan a lokacin miƙa hadaya na yamma, na tashi da ɓacin raina, da yagaggun
kayana, na durƙusa na miƙa hannuwana sama ga UBANGIJI Allahna 6 na kuma yi
addu'a, na ce,
"Ya Allah, ina cike da kunya, ba zan iya ɗaga fuskata gare ka ba, ya Allahna, domin
zunubanmu sun fi mu tsayi, tudunsu har ya kai sama. 7 Tun daga zamanin
kakanninmu har zuwa yanzu, zunubanmu suna da yawa. Domin zunubanmu, mu
da sarakunanmu, da firistocinmu aka kama mu, aka wulaƙanta mu, muka zama
bayi a hannun sarakuna waɗansu ƙasashe.
8 "Amma a yanzu a wannan ɗan lokaci UBANGIJI Allahnmu ya yi mana jinƙai, ya bar
mana saura, ya kuma ba mu wuri a wurinsa mai tsarki, ya kuma ba mu ganin
haske, ya ɗan rage mana nauyin bauta. 9 Ko da yake mu bayi ne, Allahnmu bai
yashe mu cikin daurin talala da muke ciki ba, ya sa sarakunan Farisa suka yi mana
kirki. Ya ba mu sabuwar dama don mu sāke gina haikalin Allahnmu, mu kuma
gyara katangar, ya kuma ba mu kāriya a Yahuda da Urushalima.
10 "Amma yanzu, ya Allahnmu, me za mu ce game da wannan? Gama mun ƙi bin
11 dokokin da ka bayar ta wurin annabawa lokacin da ka ce, 'Kasar da za ku
mallaka, ƙasa ce marar tsarki, mutanenta sun ɓata ta da ƙazamin hali, ƙazamin
halinsu ya ɓata ko'ina. 12 Saboda haka kada ku aurar musu da 'yan matanku, kada
kuma ku auro wa 'ya'yanku maza 'yan matansu. Kada ku yi wata yarjejjeniya ta
abokantaka da su. Idan kun yi biyayya za ku yi ƙarfi, ku kuma ci albarkar ƙasar,
har ku bar wa 'ya'yanku gādo na har abada.'
13 "Abubuwan nan sun faru da mu sakamakon mugayen ayyukanmu ne, amma duk
da haka ya Allahnmu, ba ka ba mu horo bisa ga yawan zunubanmu ba, ka kuma

bar mana saura. 14 Za mu sāke ƙin yin biyayya da umarninka mu yi aurataууa da
mutanen nan da suke aikata waɗannan abubuwan banƙyama? Ba za ka yi fushi
da mu, ka ƙone mu da fushinka har babu ɗan saura ba? 15 Ya UBANGIJI Allah na
Isra'ila, kai mai adalci ne! Yau an bar mu da sauran da ya tsira. Ga mu nan a
gabanka masu zunubi, gama ba wanda zai iya tsayawa a gabanka."

# 10

*Mutane sun furta zunubansu*

1 Yayinda Ezra yake addu'a, yake kuma furta laifi, yana kuka, yana a durƙushe da
kansa ƙasa a gaban gidan Allah, sai babban taron jama'ar Isra'ilawa, maza, mata
da yara, suka taru a wurinsa. Su ma suka yi kuka mai zafi. 2 Sai Shekaniya ɗan
Yehiyel, daga zuriyar Elam ya ce wa Ezra, "Mun yi wa Allah rashin aminci ta wurin
yin aurataууa da maƙwabtanmu, amma duk da haka bai yashe mutanen Isra'ila ba.
3 Yanzu bari mu yi alkawari da Allahnmu, mu kori matan da yaransu bisa ga abin
da ranka yă daɗe da sauran shugabannin da kuke girmama umarnin Allah kuka
shawarce mu, bari mu yi haka bisa ga doka. 4 Sai ka tashi, gama wannan hakkinka
ne, za mu ba ka goyon baya. Saboda haka ka yi ƙarfin hali ka aikata shi."
5 Sai Ezra ya tashi ya sa firistoci da suke shugabanni, da Lawiyawa, da dukan mutanen
Isra'ila su rantse, cewa za su yi abin da aka ce. Sai suka yi rantsuwar. 6 Sa'an nan
Ezra ya tashi daga gidan Allah ya tafi gidan Yehohanan ɗan Eliyashib, a can ma bai
ci wani abu ba, bai sha ruwa ba domin ya ci gaba da yin baƙin cikin rashin aminci
na waɗanda suka dawo daga bauta.
7 Aka yi shela a duk fāɗin Yahuda da Urushalima cewa dukan waɗanda suka dawo
daga bauta su tattaru a Urushalima. 8 Duk wanda bai zo a cikin kwana uku ba, za a
washe shi, a kuma ware shi daga jama'ar da suka dawo daga bauta. Haka shugabanni
da dattawa suka zartar.

9 A cikin kwana uku duk mutanen Yahuda da na Benyamin suka taru a Urushalima.
A ranar ashirin ga watan tara, dukan mutanen suka zauna a dandali a gaban gidan
Allah cike da ɓacin rai saboda abin da ya faru da kuma ruwan da aka yi. 10 Sai Ezra
firist ya miƙe tsaye ya yi musu magana ya ce, "Kun yi rashin aminci; kun aure mata
baƙi, ta haka kuka ƙara kan zunubin Isra'ila. 11 Yanzu sai ku furta zunubanku ga
UBANGIJI, Allahn kakanninku, ku kuma yi nufinsa. Ku raba kanku da mutanen da
suke kewaye da ku, ku kuma rabu da baƙin mata."
12 Mutanen kuwa suka tā da murya da ƙarfi suka ce, "Gaskiya ka faɗa, dole mu yi
yadda ka ce, 13 Amma akwai mutane da yawa, kuma lokacin damina ne; saboda haka
ba za mu iya tsayawa a waje ba. Ban da haka ma, aikin nan ba na kwana ɗaya ko
biyu ba ne, domin ba ƙaramin laifi muka yi ba. 14 Bari shugabanninmu su yi wani
abu a madadin mutane duka, sa'an nan sai duk wanda ya san ya auri baƙuwar mace
a garuruwanmu, sai yă zo nan a lokacin da aka shirya tare da dattawa da alƙalan
kowane gari, har sai Allah ya huce fushinsa mai zafi da yake kanmu." 15 Yonatan
ɗan Asahel, da Yazehiya ɗan Tikba su ne kaɗai ba su yarda da wannan shirin ba, sai
Meshullam da Shabbetai Balawe kuma suka goyi bayansu.
16 Sai waɗanda suka dawo daga bauta suka yi yadda aka zartar. Ezra firist ya zaɓi
mutane waɗanda su ne shugabannin iyalai, ɗaya daga kowane sashe, aka rubuta
sunan kowannensu. A ranar ɗaya ga watan goma kuwa suka zauna don su yi
binciken waɗannan abubuwa. 17 A rana ta farko ga watan farko, suka gama da
bincike duk waɗanda suka auri baƙin mata.

*Masu laifin aurataууa da baƙi*

18 A cikin zuriyar firistoci, ga waɗanda suka auri mata baƙi.

Daga zuriyar Yeshuwa ɗan Yozadak da ’yan’uwansa, akwai Ma’asehiya, da Eliyezer, da Yarib, da Gedaliya.
19 (Su ne suka miƙa hannuwansu suka nuna sun yarda su kori matansu baƙi, kowannensu kuma ya ba da rago daga cikin garkensa don a miƙa hadaya don zunubi.)
20 Daga zuriyar Immer, akwai
Hanani da Zebadiya.
21 Daga zuriyar Harim, akwai
Ma’asehiya, Iliya, Shemahiya, Yehiyel da Uzziya.
22 Daga zuriyar Fashhur, akwai
Eliyohenai, Ma’asehiya, Ishmayel, Netanel, Yozabad da Eleyasa.

23 Cikin Lawiyawa, akwai
Yozabad, Shimeyi, Kelaya (wato, Kelita), Fetahahiya, Yahuda, Eliyezer.
24 Daga mawaƙa, akwai
Eliyashib.
Daga masu tsaron ƙofofin haikali, akwai
Shallum, Telem da Uri.

25 Ga sunayen sauran mutanen Isra’ilan da suke da wannan laifi.
Daga zuriyar Farosh, akwai
Ramiya, da Izziya, Malkiya, Miyamin, Eleyazar, Malkiya da Benahiya.
26 Daga zuriyar Elam, akwai
Mattaniya, Zakariya, Yehiyel, Abdi, Yeremot, da Iliya.
27 Daga iyalin Zattu, akwai
Eliyohenai, Eliyashib, Mattaniya Yeremot da Zabad da Aziza.
28 Daga zuriyar Bebai, akwai
Yehohanan, Hananiya, Zabbai, da Atlai.
29 Daga zuriyar Bani, akwai
Meshullam, Malluk, Adahiya, Yashub, Sheyal, da Ramot.
30 Daga zuriyar Fahat-Mowab, akwai
Adna, Kelal, Benahiya, Ma’asehiya, Mattaniya, Bezalel, Binnuyi, da Manasse.
31 Daga zuriyar Harim, akwai
Eliyezer, Isshiya, Malkiya, Shemahiya, Simeyon,
32 Benyamin, Malluk da Shemariya.
33 Daga zuriyar Hashum, akwai
Mattenai, da Mattatta, Zabad, Elifelet, Irmai, Manasse, da Shimeyi.
34 Daga zuriyar Bani, akwai
Ma’adai, Amram, Yuwel,
35 Benahiya, Bedeya, Keluhi,
36 Baniya, Meremot, Eliyashib,
37 Mattaniya, Mattenai da Ya’asu.
38 Daga zuriyar Binnuyi, akwai
Shimeyi,
39 Shelemiya, Natan, Adahiya,
40 Maknadebai, Shashai, Sharai,
41 Azarel, Shelemiya, da Shemariya,
42 Shallum da Amariya da Yusuf.
43 Daga zuriyar Nebo, akwai
Yehiyel, Mattitiya, Zabad, Zebina, Yaddai, Yowel da Benahiya.

44 Dukan waɗannan sun auri baƙin mata, waɗansunsu suna da ’ya’ya.

# Nehemiya

*Addu'ar Nehemiya*

1 Kalmomin Nehemiya ɗan Hakaliya.

A cikin watan Kisleb a shekara ta ashirin, yayinda nake a fadar Shusha. 2 Hanani,
ɗaya daga cikin 'yan'uwana, ya zo daga Yahuda tare da waɗansu mutane. Na kuwa
tambaye shi game da raguwar Yahudawan da suka tsira daga kwasan zuwa zaman
bauta, da kuma game da Urushalima.
3 Suka ce mini, "Waɗanda suka tsira daga kwasan zuwa zaman bauta da kuma suka
komo cikin yankin suna cikin babban damuwa da wulaƙanci. An rushe katangar
Urushalima aka kuma ƙone ƙofofin da wuta."
4 Da na ji waɗannan abubuwa, sai na zauna na yi kuka. Na yi kwanaki ina makoki
da azumi, na kuma yi addu'a a gaban Allah na sama. 5 Na ce,

"Ya Ubangiji Allah na sama, Allah mai girma da mai banrazana, wanda yake
kiyaye alkawarinsa na ƙauna da waɗanda suke ƙaunarsa, suke kuma yin biyayya
da umarnansa, 6 ka sa kunne ka kuma buɗe idanunka ka ji addu'ar da bawanka
yake yi a gabanka dare da rana saboda bayinka, mutanen Isra'ila. Na furta zunuban
da mu Isra'ilawa, har da ni da kuma gidan mahaifina muka yi maka. 7 Mun yi
mugunta gare ka. Ba mu yi biyayya da umarnai, ƙa'idodi da kuma dokokin da ka
ba wa bawanka Musa ba.
8 "Ka tuna da umarnan da ka ba wa bawanka Musa, kana cewa, 'In kun yi rashin
aminci, zan warwatsar da ku a cikin al'ummai, 9 amma in kuka dawo gare ni kuka
kuma yi biyayya da umarnaina, to, ko mutanenku da aka kwasa zuwa zaman bauta
suna can wuri mafi nisa, zan tattara su daga can in kawo su wurin da na zaɓa yă
zama wurin zama don Sunana.'
10 "Su bayinka ne da kuma mutanenka da ka fansa ta wurin ƙarfinka mai girma
da kuma hannunka mai iko. 11 Ya Ubangiji, ka kasa kunne ga addu'ar wannan
bawanka da kuma ga addu'ar bayinka waɗanda suke farin cikin girmama sunanka.
Ka ba wa bawanka nasara a yau ta wurinsa yă sami tagomashi a gaban wannan
mutum."

Ni ne mai riƙon kwaf sarki.

## 2

*Artazerzes ya aiki Nehemiya Urushalima*

1 A watan Nisan a shekara ta ashirin ta mulkin Sarki Artazerzes, sa'ad aka kawo
masa ruwan inabi, sai na karɓa na ba shi. Ban taɓa ɓata fuskata a gabansa ba, sai
wannan karo. 2 Saboda haka sarki ya tambaye ni ya ce, "Me ya sa fuskarka ta ɓaci,
ga shi, ba ciwo kake ba? Ba abin da ya kawo wannan, in ba dai kana baƙin ciki ba."
Sai na ji tsoro ƙwarai, 3 na amsa na ce wa sarki, "Ran sarki yă daɗe! Me zai hana
fuskata ta ɓaci, sa'ad da birnin da aka binne kakannina tana zaman kango, aka kuma
rushe ƙofofinsa da wuta?"
4 Sai sarki ya ce mini, "Me kake so?"
Sai na yi addu'a ga Allah na sama, 5 na kuwa ba wa sarki amsa, na ce, "In ya
gamshi sarki, in kuma bawanka ya sami tagomashi a idonka, bari ka aike ni in tafi
ƙasar Yahuda, birnin da aka binne kakannina, domin in sāke gina shi."

6 Sai sarki, a lokacin sarauniya da tana zama kusa da shi, ya tambaye ni, ya ce,
"Kwana nawa tafiyar za tă ɗauke ka, kuma yaushe za ka dawo?" Ya gamshi sarki ya
aike ni; saboda haka na shirya lokaci.
7 Na kuma ce masa, "In ya gamshi sarki, zai yi kyau in sami wasiƙu zuwa ga
gwamnonin Kewayen Kogin Yuferites, domin su tanada kāriya har sai na isa Yahuda?
8 A kuma ba ni wasiƙa zuwa ga Asaf, sarkin daji, yă ba ni katako don yin ƙofofin
kagara na kusa da fadar haikali da kuma don katangar birni, da na wurin da zan
zauna?" Sarki kuwa ya ba ni abin da na roƙa, gama Allah yana tare da ni. 9 Saboda
haka na tafi wurin gwamnonin Kewayen Kogin Yuferites, na ba su wasiƙun sarki.
Sarki kuma ya aika da hafsoshin mayaƙa da kuma mahayan dawakai tare da ni.
10 Da Sanballat mutumin Horon da Tobiya wakilin ƙasar Ammon suka ji cewa wani
ya zo domin yă ƙarfafa zaman lafiyar mutanen Isra'ila, sai suka damu ƙwarai.

*Nehemiya ya dudduba katangar Urushalima*

11 Sai na je Urushalima, bayan na zauna a can na kwanaki uku, 12 sai na fita da
dare tare da mutane kalila. Ban faɗa wa wani abin da Allahna ya sa a zuciyata in yi
don Urushalima ba. Ba waɗansu dabbobi kuma tare da ni, sai dai dabbar da na hau.
13 Da dare na fita ta Kofar Kwari wajen Rijiyar Dila* da Kofar Juji, ina dudduba
katangar Urushalima waɗanda aka rushe da kuma ƙofofinta waɗanda aka ƙone da
wuta. 14 Sa'an nan na ci gaba zuwa wajen Kofar Maɓuɓɓuga da kuma Tafkin Sarki,
amma babu isashen wuri saboda abin da na hau yă bi; 15 saboda haka na haura ta
kwarin da dad dare, ina dudduba katangar. A ƙarshe, na juya na sāke shiga ta Kofar
Kwari. 16 Shugabanni ba su san inda na tafi, ko abin da nake yi ba, domin ban riga na
faɗa wa Yahudawa, ko firistoci, ko manyan gari, ko shugabanni, ko sauran waɗanda
za su yi aiki, kome ba.
17 Sai na ce musu, "Kun ga matsalar da muke ciki, yadda Urushalima ta zama kango,
an kuma ƙone ƙofofinta da wuta. Ku zo mu sāke gina katangar Urushalima, ba za
mu ƙara shan kunya ba." 18 Na kuma faɗa musu game da yadda alherin Allahna
yake tare da ni da kuma abin da sarki ya faɗa mini.
Suka amsa, suka ce, "Mu tashi, mu kama gini." Sai suka fara wannan aiki mai
kyau.
19 Amma sa'ad da Sanballat mutumin Horon da Tobiya wakilin ƙasar Ammon da
kuma Geshem mutumin Arab suka ji game da wannan, sai suka yi mana ba'a suka
kuma yi mana dariya. Suka ce, "Me kuke tsammani kuke yi? Kuna so ku yi wa sarki
tawaye ne?"
20 Na amsa musu na ce, "Allah na sama zai ba mu nasara. Mu bayinsa za mu tashi
mu fara gini, amma game da ku kam, ba ku da rabo cikin Urushalima, ba ku da wani
hakki ko wani abin tunawa."

# 3

*Masu ginin katanga*

1 Eliyashib babban firist da 'yan'uwansa firistoci suka tashi suka sāke gina Kofar
Tumaki. Suka tsarkake ta, suka sa ƙofofinta a wurarensu, suka yi ginin har
Hasumiyar Ɗari, wadda suka tsarkake, da kuma Hasumiyar Hananel. 2 Mutanen
Yeriko kuwa suka kama ginin daga mahaɗin, Zakkur ɗan Imri kuma ya fara ginin
biye da su.

3 'Ya'yan Hassenaya ne suka gina Kofar Kifi. Suka kafa ginshiƙan, suka kuma sa
ƙofofinta, da sakatunta, da kuma sandunan ƙarfenta a wurarensu. 4 Kusa da su

* **2:13** Ko kuwa Maciji ko Ɓaure

kuma, Meremot ɗan Uriya, ɗan Hakkoz ne ya yi gyare-gyaren. Biye da shi kuma sai
Meshullam ɗan Berekiya, ɗan Meshezabel ya yi gyare-gyare. Kusa da shi Zadok ɗan
Ba'ana shi ma ya yi gyare-gyare. 5 Mutanen Tekowa ne suka yi gyare-gyare biye da
shi, amma manyan garinsu suka ƙi su sa hannu cikin aikin da shugabanninsu* suka
bayar.

6 Yohiyada ɗan Faseya, da Meshullam ɗan Besodehiya ne suka gyara Kofar
Yeshana†. Suka kafa katakanta, suka sa ƙyamarenta, da sandunan ƙarfe na kulle
ƙofofinta. 7 Biye da su, mutanen Gibeyon da Mizfa Melatiya na Gibeyon da Yadon
Meronot waɗanda suke ƙarƙashin ikon gwamnan Kewayen Kogin Yuferites ne suka
yi gyare-gyaren. 8 Uzziyel ɗan Harhahiya, ɗaya daga cikin masu ƙeran zinariya ne ya
yi gyare-gyaren sashe na biye; sai Hananiya, ɗaya daga cikin masu yin turare, ya yi
gyare-gyaren biye da wannan. Suka gyara‡ Urushalima har zuwa Katanga Mai Faɗi.
9 Refahiya ɗan Hur, mai mulkin rabin yankin Urushalima, ya yi gyare-gyaren sashe
na biye. 10 Kusa da Refahiya, Yedahiya ɗan Harumaf ya yi gyare-gyaren daga gaban
gidansa, sai Hattush ɗan Hashabnehiya ya yi gyare-gyaren biye da shi. 11 Malkiya
ɗan Harim, da Hasshub ɗan Fahat-Mowab ya yi gyare-gyaren wani sashe da kuma
Hasumiyar Wurin Gashi. 12 Shallum ɗan Hallohesh, mai mulkin ɗayan rabin yankin
Urushalima ya yi gyare-gyaren sashe na biye tare da taimakon 'ya'yansa mata.

13 Hanun da mazaunan Zanowa ne suka gyara Kofar Kwari. Suka sāke gina ta
suka sa ƙofofinta, da sakatunta, da sandunan ƙarfenta a wurarensu. Suka kuma
gyara yadi ɗari biyar§ na katangar har zuwa Kofar Juji.

14 Malkiya ɗan Rekab mai mulkin yankin Bet-Hakkerem ne ya yi gyare-gyaren
Kofar Juji. Ya sāke gina ta ya kuma sa sakatunta, da sanduna ƙarfenta a wurarensu.

15 Shallum ɗan Kol-Hoze mai mulkin Mizfa ne ya yi gyare-gyaren Kofar
Maɓuɓɓuga. Ya sāke gina ta, ya yi mata jinƙa yana sa ƙofofinta, da sakatunta, da
kuma sandunan ƙarfenta a wurarensu. Ya kuma gyara katangar tafkin Silowam,* ta
Lambun Sarki, har zuwa matakalan da suka gangara daga Birnin Dawuda. 16 Gaba
da shi, Nehemiya ɗan Azbuk, mai mulkin rabin yankin Bet-Zur ne ya yi gyare-gyaren
har zuwa kusa da kaburburan† Dawuda, har zuwa haƙaƙƙen tafki da kuma Gidan
Jarumawa.
17 Biye da shi, Lawiyawa a ƙarƙashin Rehum ɗan Bani ne suka yi gyare-gyaren.
Kusa da su, Hashabiya mai mulkin rabin yankin Keyila ne ya yi gyare-gyaren don
yankinsa. 18 Biye da shi, 'yan'uwansu Lawiyawa ne a ƙarƙashin Binnuyi ɗan
Henadad, mai mulkin ɗayan rabin yankin Keyila suka yi gyare-gyaren. 19 Biye da
su, Ezer ɗan Yeshuwa, mai mulkin Mizfa, ya yi gyara wani sashe, daga inda yake
fuskantar hawan gidan makamai har zuwa kusurwa. 20 Biye da shi, Baruk ɗan Zakkai
da ƙwazo ya gyara wani sashe, daga kusurwa zuwa mashigin gidan Eliyashib babban
firist. 21 Biye da shi, Meremot ɗan Uriya, ɗan Hakkoz, ya yi gyaran wani sashe, daga
mashigin gidan Eliyashib zuwa ƙarshensa.
22 Firistoci daga kewayen yankin ne suka yi gyare-gyaren biye da shi. 23 Can gaba
da su, Benyamin da Hasshub ne suka yi gyare-gyaren a gaban gidansu, biye da su
kuwa, Azariya ɗan Ma'asehiya, ɗan Ananiya ne ya yi gyare-gyaren kusa da gidansa.

---

* 3:5 Ko kuwa shugabanninsu ko gwamna † 3:6 Ko kuwa Tsohuwar ‡ 3:8 Ko kuwa Suka bar wani sashensa § 3:13 Da Ibraniyanci kamu dubu (kamar mita ɗari huɗu da hamsin). * 3:15 Da Ibraniyanci Shela, wani sunan Shilowa, wato, Silowam. † 3:16 Da Ibraniyanci; Seftuwajin, waɗansu rubuce-rubucen hannu na Bulget da Siriyak su na da kabari ne a nan

[24] Biye da shi, Binnuyi ɗan Henadad ya yi gyaran wani sashe, daga gidan Azariya
zuwa kusurwa, [25] sai Falal ɗan Uzai ya yi aiki ɗaura da kusurwa da kuma doguwar
hasumiya daga fadar da take bisa kusa da shirayin masu tsaro. Biye da shi, Fedahiya
ɗan Farosh [26] da masu hidimar haikali da suke zama a tudun Ofel ne suka yi gyare-
gyaren har zuwa wani wuri ɗaura da Kofar Ruwa wajen gabas da kuma doguwar
hasumiya. [27] Biye da su, mutanen Tekowa suka yi gyaran wani sashe, daga babbar
doguwar hasumiya zuwa katangar Ofel.

[28] Daga Kofar Doki, firistoci ne suka yi gyare-gyaren, kowanne a gaban gidansa.
[29] Biye da su, Zadok ɗan Immer ya yi gyare-gyaren ɗaura da gidansa. Biye da shi,
Shemahiya ɗan Shekaniya, mai tsaron Kofar Gabas ya yi gyare-gyare. [30] Biye da shi,
Hananiya ɗan Shelemiya, da Hanun, ɗa na shida na Zalaf, suka gyara wani sashe.
Biye da su, Meshullam ɗan Berekiya ya yi gyare-gyaren ɗaura da wurin zamansa.
[31] Biye da shi, Malkiya, ɗaya daga cikin masu ƙera zinariya ya yi gyare-gyaren har
zuwa gidan masu hidimar haikali da kuma ʼyan kasuwa, ɗaura da Kofar Bincike, har
zuwa ɗakin da yake bisa kusurwar. [32] Maƙeran zinariya da ʼyan kasuwa suka gyara
wani sashi tsakanin ɗakin da yake bisa kusurwa da Kofar Tumaki.

# 4

*Hamayya ga sāke ginin*

[1] Da Sanballat ya ji cewa muna sāke ginin katangar, sai ya husata, ya haukace
ƙwarai. Ya yi wa Yahudawa dariya, [2] a gaban abokansa da kuma sojojin Samariya ya
ce, "Me waɗancan Yahudawan nan marasa ƙarfi suke yi? Za su maido da katangarsu
ne? Za su miƙa hadayu ne? Za su gama a rana ɗaya? Za su iya samun duwatsun gini
daga tsibin matattun duwatsu?"
[3] Tobiya wakilin mutanen Ammon wanda yake a gefensa ya ce, "Abin nan da suke
gini, ko dila ma ya hau, zai rushe shi!"

[4] Ka ji mu, ya Allahnmu, gama an rena mu. Bari zagin da suke yi mana yǎ koma
kansu. Ka sa a kwashe su a kai su bauta a wata ƙasa. [5] Kada ka rufe laifinsu, kada
kuwa ka gafarta musu, gama sun ci mutuncinmu, mu da muke gini.

[6] Sai muka sāke ginin katangar sai da duka ta kai rabin tsayinta, gama mutane sun
yi aiki da dukan ƙarfinsu.
[7] Amma da Sanballat, da Tobiya, da Larabawa, da Ammonawa, da kuma mutanen
Ashdod suka ji cewa gyare-gyaren katangar Urushalima yana cin gaba, ana kuma
tattoshe wuraren da suka tsattsaga, sai suka husata ƙwarai. [8] Dukansu suka ƙulla su
zo, su yi yaƙi da Urushalima, su tā da hankali a cikinta. [9] Amma muka yi addu'a ga
Allahnmu muka kuma sa masu tsaro da rana da kuma dare don mu magance wannan
barazana.
[10] Ana cikin haka, mutane a Yahuda suka ce, "Karfin ma'aikata yana kāsawa, akwai
kuma sauran tarkace da yawa da ba za mu iya sāke gina katangar ba."
[11] Abokan gābanmu sun ce, "Ba za su sani ba, ba kuwa za su gan mu ba, sai dai
kawai su gan mu a cikinsu, za mu karkashe su, mu tsai da aikin."
[12] Sau da yawa Yahudawan da suke da zama kusa da abokan gābanmu sun yi ta
zuwa suna yin mana magana, suna cewa "Ko'ina muka juya, za su fāɗa mana."
[13] Saboda haka na sa jama'a su ja ɗamara bisa ga iyalinsu a bayan katanga, a
wuraren da ba a gina ba. Suna riƙe da takuba, da māsu, da bakkuna. [14] Bayan na
duddduba abubuwa, sai na miƙe tsaye na ce wa manyan gari da shugabanni da kuma
sauran jama'a, "Kada ku ji tsoronsu. Ku tuna da UBANGIJI, wanda yake mai girma da

banrazana, ku yi yaƙi don ʼyanʼuwanku, da ʼyaʼyanku maza da mata, da matanku da
kuma gidajenku.”
[15] Da abokan gābanmu suka ji muna sane da shirinsu, Allah kuma ya wargaje shirin
nan, sai duk muka dawo ga katangar, kowa ya kama aikinsa.
[16] Daga wannan rana zuwa gaba, rabin mutane suka yi aiki, yayinda sauran rabin
suka kintsa da māsu, da garkuwa, da bakkuna da makamai. Shugabanni suka
goyi bayan dukan mutanen Yahuda [17] waɗanda suke ginin katanga. Waɗanda suke
ɗaukan kaya suka yi aikinsu da hannu ɗaya, suna kuma riƙe da makami a ɗaya
hannun, [18] kuma kowane mai gini ya ɗaura takobinsa a gefe yayinda yake aiki. Amma
mutum mai busa ƙaho ya kasance tare da ni.
[19] Sai na ce wa manyan gari, da shugabanni, da sauran jamaʼa, “Aikin nan babba
ne kuma mai yawa, ga shi muna a rarrabe nesa da juna a katangar. [20] Duk inda kuka
ji an busa ƙaho, sai ku taru a wurin. Allahnmu zai yi yaƙi dominmu!”
[21] Saboda haka muka ci gaba da aiki, rabin mutane suna riƙe da māsu, daga
wayewar gari har zuwa fitowar taurari. [22] A wannan lokaci na kuma ce wa mutane,
“A sa kowane mutum da mataimakinsa su zauna a Urushalima da dare, domin a yi
tsaro da dare, da safe kuma a kama aiki.” [23] Saboda haka ni, da ʼyanʼuwana, da
bayina, da matsaran da suke tare da ni, ba wanda ya tuɓe tufafinsa; kowa ya rataye
makaminsa, ko ya je shan ruwa ma.*

# 5

*Nehemiya ya taimaki matalauta*

[1] To, sai maza da matansu suka tā da fara gunaguni mai tsanani a kan ʼyanʼuwansu
Yahudawa. [2] Waɗansu suka ce, “Mu da ʼyaʼyanmu maza da mata muna da yawa,
muna bukatar hatsi domin mu ci mu rayu.”
[3] Waɗansu kuwa suka ce, “Saboda yunwa mun jinginar da gonakinmu, da gonakin
inabinmu, da gidajenmu don mu sami hatsi.”
[4] Har illa yau waɗansu suka ce, “Mun ci bashin kuɗi don mu biya haraji a
kan gonakinmu, da gonakin inabinmu. [5] Ga shi kuwa, mu da su dangin juna ne,
ʼyaʼyanmu da nasu kuma ɗaya ne, duk da haka an tilasta mu mu sa ʼyaʼyanmu mata
da maza su zama bayi. Har ma an riga an bautar waɗansu daga cikin ʼyaʼyanmu
mata, amma ba mu da iko mu ce kome, domin gonakinmu da gonakin inabinmu
suna a hannun waɗansu mutane.”
[6] Saʼad da na ji kukansu da waɗannan koke-koke, na husata ƙwarai. [7] Na yi
tunaninsu a zuciyata saʼan nan na zargi manyan gari da shugabanni. Na ce musu,
“Kuna musguna wa ʼyanʼuwanku ta wurin ba su rance da ruwa!” Saboda haka
na kira babban taro gaba ɗaya don a magance wannan. [8] Na ce, “Da dukan
iyakar ƙoƙarinmu, mun fanshi ʼyanʼuwanmu Yahudawan da aka sayar wa Alʼummai.
Amma ga shi kuna sayar da ʼyanʼuwanku ga Alʼummai, don kawai a sāke sayar mana
da su!”
[9] Saboda haka na ci gaba na ce, “Abin da kuke yi a yanzu ba daidai ba ne. Bai
kamata ku yi tafiya cikin tsoron Allahnmu don mu guji baʼar Alʼummai abokan
gābanmu ba? [10] Ni ma da ʼyanʼuwana da kuma mutanena muna ba wa mutane
bashin kuɗi da kuma hatsi. Sai mu daina shaʼanin ba da rance da ruwa! [11] Yau sai
ku mayar musu da gonakinsu, da gonakin inabinsu, da na zaitunsu, da gidajensu, da
kashi ɗaya bisa ɗari na kuɗi, da na hatsi, da na ruwan inabi, da na mai, waɗanda
kuka karɓa a wurinsu.”
[12] Suka ce, “Za mu mayar musu, kuma ba za mu bukaci wani abu daga gare su ba.
Za mu yi yadda ka faɗa.”

* **4:23** Maʼanar Ibraniyanci na wannan jumla ba a tabbatar ba.

Sai na tattara firistoci na kuma sa manyan gari da shugabanni su yi rantsuwa don
su yi abin da suka yi alkawari. 13 Na kuma kakkaɓe hannuna, na ce, “Duk wanda ya
karya wannan alkawari, haka Allah zai kakkaɓe shi daga gidansa da aikinsa. Allah
zai kakkaɓe shi, yă wofintar da shi!”

Da jin wannan, sai dukan taron suka ce, “Amin,” suka kuma yabi UBANGIJI. Mutane
kuwa suka yi kamar yadda suka yi alkawari.

14 Ban da haka ma, daga shekara ta ashirin ta Sarki Artazerzes, sa’ad da aka naɗa
ni in zama gwamnansu a ƙasar Yahuda, har zuwa shekara ta talatin da biyu na
mulkinsa, shekara sha biyu ke nan, ko ni, ko ’yan’uwana, ba wanda ya ci abincin da
akan ba wa gwamna. 15 Amma gwamnonin farko, waɗanda suka riga ni, sun ɗaura
wa mutane kaya mai nauyi suka karɓi shekel arba’in na azurfa daga gare su haɗe
da abinci da kuma ruwan inabi. Har bayin masu mulki ma sun nawaya wa mutane.
Amma ni ban yi haka ba, saboda ina tsoron Allah. 16 A maimakon haka, na miƙa
kaina ga aiki a kan wannan katanga. Na tattara dukan mutanena a can don aikin;
ba mu samar wa kanmu wata gona ba.

17 Bugu da ƙari, Yahudawa da shugabanni ɗari da hamsin suna ci daga teburina,
haka ma waɗanda suka zo wurinmu daga ƙasashen da suke kewaye. 18 Kowace
rana akan shirya mini saniya ɗaya, zaɓaɓɓun tumaki shida da waɗansu kaji, kuma
kowace kwana goma akan tanadar da ruwan inabi na kowane iri a yalwace. Duk da
haka, ban taɓa nemi a ba ni abincin da akan ba wa gwamna ba, domin wahala ta yi
wa jama’a yawa.

19 Ka tuna da ni, ka yi mini alheri, ya Allah, saboda dukan abubuwan da na yi
saboda waɗannan mutane.

# 6

*Ci gaba da hamayya ga sāke yin gini*

1 Sa’ad da magana ta zo kunnen Sanballat, da Tobiya, da Geshem mutumin Arab da
kuma sauran abokan gābanmu cewa na sāke gina katangar har babu sauran tsaguwa
da ta ragu, ko da yake har zuwa lokacin ban sa ƙofofi a ƙyamare ba 2 Sanballat da
Geshem suka aika mini wannan saƙo cewa, “Ka zo, mu sadu a wani ƙauye a filin
Ono.”

Amma makirci ne suke yi don su cuce ni; 3 saboda haka sai na aika musu da wannan
amsa, na ce, “Ina cikin babban aiki, ba zan kuwa iya gangarawa ba. Don me zan bar
aikin yă tsaya don in gangara zuwa wurinku?” 4 Suka yi ta aiko mini da wannan
saƙo har sau huɗu, ni kuwa na yi ta ba su amsa irin ta dā.

5 Sai sau na biya, Sanballat ya aiki mataimakinsa gare ni da irin saƙo guda, kuma
a hannunsa akwai wasiƙar da ba a yimƙe ba 6 wadda aka rubuta cewa,

“An ba da labari cikin al’ummai, kuma Geshem ya ce gaskiya ne, cewa kai da
Yahudawa kun shirya tawaye, saboda haka kuke sāke ginin katangar. Ban da haka
ma, bisa ga waɗannan rahotanni kana shirin zaman sarkinsu 7 har ma ka naɗa
annabawa su yi wannan shela game da kai a Urushalima, su ce, ‘Akwai sarki a
Yahuda!’ To, wannan rahoto zai koma wurin sarki; saboda haka ka zo, mu tattauna
wannan batu.”

8 Sai na aika masa wannan amsa, na ce, “Babu wani abu haka da yake faruwa; ka
dai ƙaga wannan daga tunaninka ne.”

9 Suka dai yi ƙoƙari su tsoratar da mu, suna cewa, “Hannuwansu za su rasa ƙarfin
yin aiki, ba kuwa za su ƙare aikin ba.”

Amma na yi addu’a na ce, “Yanzu, ya Allah, ka ƙarfafa hannuwana.”

10 Wata rana na tafi gidan Shemahiya ɗan Delahiya, ɗan Mehetabel, wanda aka
hana fita a gidansa. Ya ce mini, “Mu sadu gobe a gidan Allah, a cikin haikali, mu

kuma kulle ƙofofin haikali, gama mutane suna zuwa su kashe ka, tabbatacce za su
zo da dare su kashe ka.”
11 Amma na ce, “Ya kamata mutum kamar ni yă gudu? Ko kuwa ya kamata wani
kamar ni yă shiga cikin haikali don yă ceci ransa? Ba zan tafi ba!” 12 Na gane cewa
Allah bai aike shi ba, ya yi annabci a kaina domin Tobiya da Sanballat sun yi hayarsa
ne. 13 An yi hayarsa don yă sa in ji tsoro in yi zunubi ta yin haka, sa’an nan za su ba
ni mugun suna, su wofinta ni.

14 Ya Allahna, ka tuna da Tobiya da Sanballat, saboda abin da suka yi; ka kuma
tuna da annabiya Nowadiya da sauran annabawa waɗanda suke ƙoƙari su tsorata
ni.

### *Gamawar katanga*

15 Cikin kwana hamsin da biyu aka gama gina katangar, a ranar ashirin da biyar
ga watan Elul. 16 Sa’ad da dukan abokan gābanmu suka ji haka, dukan al’umman
da suke kewaye da mu suka ji tsoro, suka rasa ƙarfin halinsu, domin sun gane cewa
wannan aiki an yi shi da taimakon Allahnmu ne.
17 A waɗannan kwanaki, manyan garin Yahuda suka yi ta aika wasiƙu masu yawa
zuwa ga Tobiya, shi kuma ya yi ta aika musu da amsoshi. 18 Gama mutane da yawa a
cikin Yahuda sun rantse wa Tobiya za su goyi bayansa, domin ya auri ’yar Shekaniya,
ɗan Ara. Ɗansa kuma, wato, Yehohanan, ya auri ’yar Meshullam, ɗan Berekiya.
19 Ban da haka ma, mutanen sun yi ta ba ni labarin ayyuka masu kyau da Tobiya
ya yi, sa’an nan kuma suna faɗa masa duk abin da na faɗa. Tobiya kuwa ya aika
wasiƙu don yă tsorata ni.

## 7

1 Bayan an sāke gina katangar na kuma sa ƙofofi a wurarensu, sai aka naɗa masu
tsaro, da mawaƙa, da Lawiyawa. 2 Na sa ɗan’uwana Hanani tare da Hananiya
shugaban fada aikin riƙon Urushalima, domin shi Hananiya mutum mai mutunci
ne, mai tsoron Allah fiye da yawancin mutane. 3 Na ce musu, “Kada a buɗe ƙofofin
Urushalima da sassafe sai rana ta fito sosai. Yayinda matsaran ƙofofi suna aiki, a
kulle ƙofofin a sa musu sakata kafin matsaran su tashi, wajen fāɗuwar rana. Ku
kuma naɗa mazaunan Urushalima a matsayin masu tsaro, waɗansunsu a wuraren
aiki, waɗansun kuma kusa da gidajensu.”

### *Jerin sunayen waɗanda aka kai bauta da suka dawo (Ezra 2.1-70)*

4 Birnin Urushalima kuwa tana da fāɗi da girma, amma mutanen da suke zama
a cikinta kaɗan ne, ba a kuma gina gidaje da yawa ba tukuna. 5 Sai Allahna ya sa
a zuciyata in tara manyan gari, shugabanni da talakawa don a rubuta su bisa ga
iyalansu. Na sami littafin asali na waɗanda suka fara dawowa. Ga abin da na tarar
an rubuta a ciki.

> 6 Waɗannan su ne mutanen yankin da suka dawo daga zaman bautar da
> Nebukadnezzar sarkin Babilon ya kame (sun dawo Urushalima da Yahuda,
> kowanne zuwa garinsa. 7 Sun dawo tare da Zerubbabel, da Yeshuwa,
> da Nehemiya, da Azariya, da Ra’amiya, da Nahamani, da Mordekai, da
> Bilshan, da Misfar, da Bigwai, da Nehum da kuma Ba’ana).

Ga jerin mutanen Isra’ila.

8 Zuriyar
Farosh mutum 2,172

9 ta Shefatiya 372
10 ta Ara 652
11 ta Fahat-Mowab (ta wurin Yeshuwa da Yowab) 2,818
12 ta Elam 1,254
13 ta Zattu 845
14 ta Zakkai 760
15 ta Binnuyi 648
16 ta Bebai 628
17 ta Azgad 2,322
18 ta Adonikam 667
19 ta Bigwai 2,067
20 ta Adin 655
21 ta Ater (ta wurin Hezekiya) 98
22 ta Hashum 328
23 ta Bezai 324
24 ta Harif 112
25 ta Gibeyon 95.
26 Mutanen
Betlehem da na Netofa 188
27 na Anatot 128
28 na Bet-Azmawet 42
29 na Kiriyat Yeyarim, Kefira da na Beyerot 743
30 na Rama da na Geba 621
31 na Mikmash 122
32 na Betel da na Ai 123
33 na ɗayan Nebo 52
34 na ɗayan Elam 1,254
35 na Harim 2 320
36 na Yeriko 345
37 na Lod, da na Hadid, da na Ono 721
38 na Sena'a 3,930.

39 Ga zuriyar Firistoci.
Zuriyar
Yedahiya (ta wurin iyalin Yeshuwa) 973
40 ta Immer 1,052
41 ta Fashhur 1,247
42 ta Harim 1,017.

43 Ga zuriyar Lawiyawa.
Zuriyar
Yeshuwa da Kadmiyel (ta wurin Hodeba) 74.

44 Mawaƙa.
Zuriyar
Asaf mutum 148.

45 Ga zuriyar Matsaran Kofofi.
Zuriyar
Shallum, Ater, Talmon,
Akkub, Hatita da Shobai 138.

46 Ma'aikatan haikali.
Zuriyar

Ziha, Hasufa, Tabbawot,
47 da ta Keros, da ta Siya, da ta Fadon,
48 da ta Lebana, da ta Hagaba, da ta Shalmai,
49 da ta Hanan, da ta Giddel, da ta Gahar,
50 da ta Reyahiya, da ta Rezin, da ta Nekoda,
51 da ta Gazzam, da ta Uzza, da ta Faseya,
52 da ta Besai, da ta Meyunawa, da ta Nefussiyawa,
53 da ta Bakbuk, da ta Hakufa, da ta Harhur,
54 da ta Bazlit, da ta Mehida, da ta Harsha,
55 da ta Barkos, da ta Sisera, da ta Tema,
56 da ta Neziya, da kuma ta Hatifa.
57 Ga zuriyar bayin Solomon.
Zuriyar
Sotai, da ta Soferet, da ta Ferida,
58 da ta Ya'ala, da ta Darkon, da ta Giddel,
59 Shefatiya, Hattil,
Fokeret-Hazzebayim, da Amon.
60 Zuriyar ma'aikatan haikali da ta bayin Solomon su 392.

61 Waɗansu sun hauro daga garuruwan Tel-Mela, Tel-Harsha, Kerub, Addon da Immer, amma ba su iya nuna cewa iyalansu su zuriyar Isra'ila ce ba,
62 zuriyar
Delahiya, Tobiya, da Nekoda 642.

63 Na wajen firistoci kuwa su ne,
Zuriyar
Hobahiya, da ta Hakkoz, da ta Barzillai (wani mutumin da ya auri 'yar Barzillai mutumin Gileyad, aka kuma kira shi da wannan suna).
64 Waɗannan ne aka nemi sunayensu a cikin tarihin asalin iyalai, amma ba a same su a ciki ba, saboda haka aka hana su shiga cikin firistoci, sun zama kamar marasa tsarki. 65 Sai gwamna ya umarce su kada su ci wani abinci mafi tsarki, sai akwai firist da zai nemi nufin UBANGIJI ta wurin Urim da Tummim.

66 Yawan jama'ar duka ya kai mutum 42,360, 67 ban da bayinsu maza da mata 7,337. Suna kuma da mawaƙa maza da mata 245. 68 Akwai dawakai 736, alfadarai 245 69 raƙuma 435, da kuma jakuna 6,720.

70 Waɗansu shugabannin iyalai suka ba da kyautai domin taimakon aiki. Gwamna ya ba da darik 1,000 na zinariya, kwanoni 50, da riguna 530 don firistoci.
71 Waɗansu shugabannin iyalai sun ba da darik 20,000 na zinariya da mina 2,200
na azurfa don aiki. 72 Jimillar da sauran mutane suka bayar ta kai darik 20,000 na
zinariya, minas 2,000 na azurfa, da riguna sittin da bakwai don firistoci.
73 Firistoci, da Lawiyawa, da matsaran ƙofofi, da mawaƙa, da ma'aikatan haikali tare da waɗansu mutane da kuma sauran mutanen Isra'ila, suka zauna a garuruwansu.

### *Ezra ya karanta Doka*

Da wata na bakwai ya zo, Isra'ilawa kuwa sun riga sun zauna a garuruwansu,

# 8

1 sai dukan mutane suka taru kamar mutum guda a dandali a gaban Kofar Ruwa.
Suka faɗa wa Ezra malamin Doka yă fitar da Littafin Dokar Musa, wanda Ubangiji
ya umarta domin Isra'ila.

2 Saboda haka a rana ta farko ga watan bakwai, Ezra firist, ya kawo Doka a gaban
taro, wanda ya ƙunshi maza da mata da dukan waɗanda za su iya fahimta. 3 Ya
karanta Dokar da ƙarfi daga safe har tsakar rana yayinda yake a kan dandali da yake
fuskantar dandali a gaban Kofar Ruwa, gaban maza, mata da kuma sauran mutanen
da za su iya fahimta. Dukan mutane kuwa suka saurara a hankali ga karatun Littafin
Dokar.

4 Ezra malamin Doka ya tsaya a kan dakalin itacen da aka yi saboda wannan hidima.
Kusa da shi a damansa, Mattitiya, Shema, Anahiya, Uriya, Hilkiya da Ma'asehiya
suka tsaya; a hagunsa kuma Fedahiya, Mishayel, Malkiya, Hashum, Hashbaddana,
Zakariya da Meshullam suka tsaya.

5 Sai Ezra ya buɗe littafin. Dukan mutane kuwa suka gan shi domin yana tsaye a
bisa fiye da inda mutane suke tsaye; yayinda ya buɗe littafin kuwa, dukan mutane
suka miƙe tsaye. 6 Ezra ya yabi Ubangiji, Allah mai girma; dukan mutane kuwa suka
tā da hannuwansu suka amsa, "Amin! Amin!" Sa'an nan suka sunkuya suka yi wa
Ubangiji sujada da fuskokinsu har ƙasa.

7 Lawiyawa, wato, su Yeshuwa, Bani, Sherebiya, Yamin, Akkub, Shabbetai, Hodiya,
Ma'asehiya, Kelita, Azariya, Yozabad, Hanan da Felahiya, suka koyar da mutane a
cikin Dokar yayinda mutane suke a tsaye a can. 8 Suka karanta daga Littafin Dokar
Allah, suna sa kowa ya gane, suna kuma ba da fassarar domin mutane su fahimci
abin da ake karatu.

9 Sa'an nan Nehemiya gwamna, Ezra firist da kuma wanda yake malamin Doka, da
Lawiyawa waɗanda suke koyar da mutane, suka ce musu duka, "Wannan rana mai
tsarki ce ga Ubangiji Allahnku. Kada ku yi makoki ko kuka." Gama dukan mutane
suna ta kuka yayinda suke sauraran kalmomin Dokar.

10 Nehemiya ya ce, "Ku koma gidajenku ku ci abinci mai kyau, ku sha abin sha
mai zaƙi, ku kuma aika wa wanda ba shi da shi. Wannan rana mai tsarki ce ga
Ubangijinmu. Kada ku yi baƙin ciki, gama farin cikin Ubangiji shi ne ƙarfinku."

11 Lawiyawa suka rarrashi mutane duka suna cewa, "Ku natsu, gama wannan rana
ce mai tsarki. Kada ku yi baƙin ciki."

12 Sa'an nan dukan mutane suka koma gidajensu suka ci, suka sha, suka aika wa
wanda ba shi da abinci, gama yanzu sun fahimci kalmomin da aka karanta musu.

13 A rana ta biyu ga wata, shugabannin iyalai, tare da firistoci da Lawiyawa, suka
taru kewaye da Ezra malamin Doka don su mai da hankali ga kalmomin Dokar.
14 Suka tarar a rubuce a cikin Doka wadda Ubangiji ya umarta ta wurin Musa, cewa
Isra'ilawa su zauna a bukkoki a lokaci bikin watan bakwai 15 kuma cewa ya kamata
su yi shelar wannan magana, su kuma yaɗa ta a duk garuruwansu da kuma cikin
Urushalima cewa, "Ku fita zuwa cikin ƙasar tudu ku kawo rassa daga itatuwan zaitun
da na zaitun jeji, da kuma daga dargaza, da dabino da itatuwa masu ganye, don yin
bukkoki", kamar yadda yake a rubuce.

16 Sai mutanen suka fita suka dawo da rassa suka kuma yi wa kansu bukkoki a
bisa rufin ɗakunansu, a cikin filaye, a shirayin gidan Allah, da ciki dandalin da yake
kusa da Kofar Ruwa, da kuma a dandalin da yake a Kofar Efraim. 17 Dukan jama'ar
da suka komo daga zaman bauta suka yi bukkoki suka kuma zauna a cikinsu. Daga
kwanakin Yoshuwa ɗan Nun har yă zuwa yau, Isra'ilawa ba su taɓa yin bikinsa haka
ba. Mutane suka cika da farin ciki sosai.

18 Kowace rana, daga rana farko zuwa ƙarshe, Ezra ya karanta daga Littafin Dokar
Allah. Suka yi bikin kwana bakwai, a rana ta takwas kuma suka yi muhimmin taro
bisa ga ƙa'ida.

# 9

*Isra'ilawa sun furta zunubansu*

1 A rana ta ashirin da huɗu ga watan nan, Isra'ilawa suka taru, suna yin azumi,
suna sa rigunan makoki, suna kuma zuba toka a kansu. 2 Waɗanda suke zuriyar
Isra'ilawa suka ware kansu daga dukan baƙi. Suka tsaya, suka kuma furta zunubansu
da muguntar kakanninsu. 3 Sa'ad da suke nan a tsaye, aka ɗauki awa uku ana
karanta Littafin Dokar UBANGIJI Allahnsu. Aka kuma ɗauki awa uku ana sujada ga
UBANGIJI Allahnsu. 4 A kan dakalin kuwa akwai Lawiyawa, wato, Yeshuwa, Bani,
Kadmiyel, Shebaniya, Bunni, Sherebiya, Bani da Kenani tsaye, waɗanda suka kira
da babbar murya ga UBANGIJI Allahnsu. 5 Lawiyawan nan, Yeshuwa, Kadmiyel, Bani,
Hashabnehiya, Sherebiya, Hodiya, Shebaniya da Fetahahiya, suka ce, “Ku miƙe tsaye
ku yabi UBANGIJI Allahnku, wanda yake har abada abadin.”

“Albarka ta tabbata ga sunanka mai ɗaukaka, bari kuma a ɗaukaka shi bisa
dukan albarka da yabo. 6 Kai kaɗai ne UBANGIJI. Kai ka yi sammai, har ma da
sama sammai, da dukan rundunar taurari, da duniya da kuma dukan abin da yake
cikinta, da tekuna da dukan abubuwan da suke cikinsu. Ka ba da rai ga kome,
kuma rundunonin sama suna maka sujada.

7 “Kai ne UBANGIJI Allah, wanda ya zaɓi Abram, ya fitar da shi daga Ur na
Kaldiyawa, ya kuma ba shi suna Ibrahim. 8 Kai ka sami zuciyarsa da aminci a
gare ka, ka kuma yi alkawari da shi cewa za ka ba zuriyarsa ƙasar Kan'aniyawa,
da ta Hittiyawa, da ta Amoriyawa, da ta Ferizziyawa, da ta Yebusiyawa, da kuma
ta Girgashiyawa. Ka kiyaye alkawarinka domin kai mai adalci ne.

9 “Ka ga wahalar kakanninmu a Masar; ka kuwa ji kukansu a Jan Teku.
10 Ka aika da alamu masu banmamaki da al'ajabai a kan Fir'auna, a kan dukan
shugabanninsa da kuma a kan dukan mutanen ƙasarsa, gama ka ga irin danniyar
da suka yi wa mutanenka. Ka samo wa kanka suna, wadda ta dawwama har
yă zuwa yau. 11 Ka raba teku a gaban kakanninmu, saboda su wuce cikinsa a
busasshiyar ƙasa, amma ka hallaka masu binsu cikin zurfafa, nutse kamar dutse
a cikin ruwa. 12 Da rana ka bishe kakanninmu da girgije, da dare kuwa ka bishe
su da ginshiƙin wuta don ka ba su haske a hanyar da za su bi.

13 “Ka sauko a kan Dutsen Sinai; ka yi musu magana daga sama. Ka ba su ƙa'idodi
da dokokin da suke masu adalci da kuma daidai, ka ba su farillai da umarnai da
suke da kyau. 14 Ka sanar da su Asabbacinka mai tsarki, ka kuma ba su umarnai,
da farillai, da kuma dokoki ta wurin bawanka Musa. 15 Cikin yunwansu ka ba su
burodi daga sama, cikin ƙishirwansu kuma ka fitar musu ruwa daga dutse. Ka
faɗa musu su shiga su mallaki ƙasar da ka rantse ta wurin ɗaga hannu cewa za
ka ba su.

16 “Amma su kakanninmu, suka yi fariya da taurinkai, ba su kuwa yi biyayya
ga umarnanka ba. 17 Suka ƙi su saurare ka, suka kāsa tuna da mu'ujizan da ka
aikata a cikinsu. Suka yi taurinkai, cikin tawayensu kuma suka naɗa shugaba don
su koma bautarsu. Amma kai Allah ne mai gafartawa, mai alheri da jinƙai, mai
jinkirin fushi, mai yalwar ƙauna. Saboda haka ba ka yashe su ba, 18 ko ma sa'ad
da suka yi wa kansu siffar ɗan maraƙi, suka ce, ‘Wannan shi ne allahnku, wanda
ya fitar da ku daga Masar,’ ko sa'ad da suka yi saɓo mai bantsoro.

19 “Saboda jinƙanka mai girma, ba ka yashe su a hamada ba. Da rana, ginshiƙin
girgije bai daina bishe su a hanyarsu ba, da dare kuma ginshiƙin wuta bai daina

haskakawa a hanyar da za su bi ba. 20 Ka ba da Ruhunka mai kyau don yă koyar
da su. Ba ka janye Manna naka daga bakunansu ba, ka kuma ba su ruwa don
ƙishirwansu. 21 Shekaru arba'in ka riƙe su a cikin hamada; ba su rasa kome ba,
rigunansu ba su yage ba, ƙafafunsu kuwa ba su kumbura ba.

22 "Ka ba su mulkoki da al'ummai, kana ba su har ma da ƙasashen da suke jeji.
Suka ci ƙasar Sihon na sarkin Heshbon da ƙasar Og inda sarkin Bashan yake mulki.
23 Ka sa 'ya'yansu maza suka yi yawa kamar taurarin sararin sama, ka kuma kawo
su cikin ƙasar da ka faɗa wa kakanninsu su shiga su mallake. 24 'Ya'yansu maza
suka shiga suka kuma mallaki ƙasar. A gabansu ka rinjayi Kan'aniyawan da suke
zama a cikin ƙasar; ka ba da Kan'aniyawa a gare su, tare da sarakunansu da kuma
mutanen ƙasar, su yi da su yadda suke so. 25 Suka kame birane masu katanga
masu ƙarfi, da ƙasa masu ba da amfani; suka mallaki gidaje cike da kowane irin
abu mai kyau, da rijiyoyin da aka riga aka haƙa, da gonakin inabi, da gonakin
itatuwan zaitun da kuma itatuwan ba da 'ya'ya a yalwace a ciki. Suka ci suka
ƙoshi, suka kuma yi ƙiba; suka ji daɗi cikin alherinka mai girma.

26 "Amma suka yi rashin biyayya suka kuma yi tawaye gare ka; suka sa dokarka
a bayansu. Suka kashe annabawanka waɗanda suka gargaɗe su don su mai da
su gare ka; suka aikata saɓo mai bantsoro. 27 Saboda haka ka miƙa su ga abokan
gābansu waɗanda suka yi musu danniya. Amma sa'ad da ake danniyarsu sai suka
yi kuka gare ka. Daga sama ka ji su, cikin jinƙanka mai girma kuwa ka ba su mai
ceto, wanda ya fisshe su daga hannun abokan gābansu.

28 "Amma nan da nan, da suka sami hutu, sai suka sāke aikata abin da yake
mugu a idonka. Sai ka yashe su ga hannun abokan gābansu don su yi mulki a
kansu. Sa'ad da suka yi kuka kuma gare ka, ka ji daga sama, cikin jinƙanka kuma
ka fisshe su sau da sau.

29 "Ka gargaɗe su su dawo ga dokarka, amma suka yi fariya, suka bijire wa
umarnanka. Suka yi zunubi game da farillanka waɗanda ta wurinsu ne mutum
zai rayu in ya yi biyayya da su. Cikin taurinkai suka juye bayansu daga gare ka,
suka zama masu taurinkai, suka kuma ƙi su saurara. 30 Shekaru masu yawa ka yi
haƙuri da su. Ta wurin Ruhunka ka gargaɗe su ta wurin annabawa. Duk da haka
ba su kasa kunne ba, saboda haka ka miƙa su ga maƙwabtansu. 31 Amma cikin
tausayinka mai girma ba ka kawo su ga ƙarshe ko ka yashe su ba, gama kai Allah
ne mai alheri da kuma mai jinƙai.

32 "To yanzu, ya Allahnmu, mai girma, mai iko, da kuma mai banrazana,
wanda yake kiyaye alkawarinsa na ƙauna, kada ka bar dukan wannan wahala
ta zama kamar marar muhimmanci a idanunka, wahalar da ta zo a kanmu, a kan
sarakunanmu da shugabanni, a kan firistocinmu da annabawa, a kan kakanninmu
da kuma dukan mutanenka, daga kwanakin sarakunan Assuriya har yă zuwa yau.
33 Cikin dukan abubuwan da suka faru da mu, ka kasance mai adalci; ka yi aminci,
yayinda mu kuwa muka aikata mugu. 34 Sarakunanmu, da shugabanninmu, da
firistocinmu da kuma kakanninmu ba su bi dokarka ba, ba su ma mai da hankali ga
umarnanka ko gargaɗin da ka yi musu ba. 35 Ko ma yayinda suke a masarautarsu,
suna jin daɗin girmar kyautatawarka gare su, cikin ƙasar mai girma, da kuma mai
fāɗin da ka ba su, ba su bauta maka ko su juye daga mugayen hanyoyinsu ba.

36 "Amma duba, mu bayi ne a yau, bayi a ƙasar da ka ba kakanninmu don su
ci amfaninta da kuma waɗansu abubuwa masu kyau da take bayarwa. 37 Saboda
zunubanmu, yalwar girbin da muke samu yana tafiya wurin sarakunan da ka sa a
kanmu. Suna mulki bisa jikunanmu, da bisa garkenmu yadda suka ga dama. Muna
cikin baƙin ciki.

### *Alkawarin mutane*

38 “Saboda wannan duka, muna yin zaunannen alkawari, muna sa shi a rubuce, shugabanninmu kuwa da Lawiyawanmu, da firistocinmu suna buga hatimansu a kai.”

# 10

1 Waɗanda suka buga hatimin su ne,

Nehemiya ɗan Hakaliya, wanda yake gwamna.

Zedekiya 2 da Serahiya, da Azariya, da Irmiya,
3 da Fashhur, da Amariya, da Malkiya,
4 da Hattush, da Shebaniya, da Malluk,
5 da Harim, da Meremot, da Obadiya,
6 da Daniyel, da Ginneton, da Baruk,
7 da Meshullam, da Abiya, da Miyamin,
8 da Ma’aziya, da Bilgai, da kuma Shemahiya.
Waɗannan su ne Firistocin.

9 Lawiyawan kuwa su ne,
Yeshuwa ɗan Azaniya, da Binnuyi ɗan Henadad, da Kadmiyel,
10 ’yan’uwansu kuwa su ne, Shebaniya,
da Hodiya, da Kelita, da Felahiya, da Hanan,
11 da Mika, da Rehob, da Hashabiya,
12 da Zakkur, da Sherebiya, da Shebaniya,
13 da Hodiya, da Bani da kuma Beninu.

14 Shugabannin mutane su ne,
Farosh, da Fahat-Mowab, da Elam, da Zattu, da Bani,
15 da Bunni, da Azgad, da Bebai,
16 da Adoniya, da Bigwai, da Adin,
17 da Ater, da Hezekiya, da Azzur,
18 da Hodiya, da Hashum, da Bezai,
19 da Harif, da Anatot, da Nebai,
20 da Magfiyash, da Meshullam, da Hezir,
21 da Meshezabel, da Zadok, da Yadduwa
22 da Felatiya, da Hanan, da Anahiya,
23 da Hosheya, da Hananiya, da Hasshub,
24 da Hallohesh, da Filha, da Shobek,
25 da Rehum, da Hashabna, da Ma’asehiya
26 da Ahiya, da Hanan, da Anan,
27 da Malluk, da Harim da kuma Ba’ana.

28 “Sauran mutane, wato, firistoci, Lawiyawa, matsaran ƙofofi, mawaƙa, ma’aikatan haikali da dukan waɗanda suka ware kansu daga maƙwabta saboda Dokar Allah, tare da matansu da dukan ’ya’yansu maza da mata waɗanda za su iya fahimta, 29 dukan waɗannan yanzu suka sadu da manyan gari ’yan’uwansu,
suka rantse, cewa la’ana ta same su idan ba su kiyaye Dokar Allah da aka bayar ta wurin Musa bawan Allah su kuma mai da hankali ga yin biyayya da dukan umarnai, ƙa’idodi da farillan Ubangiji shugabanmu ba.

[30] “Mun yi alkawari ba za mu ba da ’ya’yanmu mata aure ga mutanen da suke
kewaye da mu ba, ba kuwa za mu auri ’ya’yansu mata wa ’ya’yanmu maza ba.

[31] “Sa’ad da maƙwabta suka kawo kayayyaki ko hatsi don su sayar a ranar
Asabbaci, ba za mu saya daga gare su a ranar Asabbaci ko a rana mai tsarki ba.
Kowace shekarar Asabbaci ba za mu nome ƙasa ba kuma za mu yafe kowane irin
bashi.

[32] “Mun ɗauka hakkin bin umarnai na ba da kashi ɗaya bisa uku na shekel
kowace shekara don hidimar gidan Allahnmu. [33] Za mu tanada burodin da ake
ajiye a kan tebur; za mu ba da hadayun hatsi da hadayun ƙonawa na kullum; za
mu ba da hadayun Asabbatai, da na bukukkuwan Sabon Wata da na bukukkuwan
da aka ƙayyade; za mu ba da hadayu masu tsarki; za mu ba da hadayun zunubi
don a yi kafara domin Isra’ila; mu kuma ba da abubuwan da ake bukata dukan
domin ayyukan gidan Allahnmu.

[34] “Mu, firistoci, da Lawiyawa da kuma mutane, mun jefa ƙuri’a don a san lokacin
da kowane iyalinmu zai kawo sadakar itace don ƙonewa a gidan Allahnmu a
ƙayyadaddun lokuta a bagaden UBANGIJI Allahnmu, kamar yadda yake a rubuce a
cikin Doka.

[35] “Mun kuma ɗauka hakkin kawo nunan fari na hatsinmu da kuma na kowane
itace mai ba da ’ya’ya a gidan UBANGIJI kowace shekara.

[36] “Kamar yadda yake a rubuce a cikin Doka,* za mu kawo ɗan fari na ’ya’yanmu
maza da na garken shanunmu, da na tumakinmu, da kuma na awakinmu a gidan
Allahnmu, don firistocin da suke aikin a can.

[37] “Ban da haka ma, za mu kawo wa ɗakunan ajiyar gidan Allahnmu, abincinmu
na farko daga ƙasa, na hadayun hatsinmu, na ’ya’yan dukan itatuwanmu da
kuma na sabon ruwan inabinmu da mai namu wa firistoci. Za mu kuma kawo
zakkar hatsinmu wa Lawiyawa, gama Lawiyawa ne ke karɓan Zakka cikin dukan
garuruwan da muke noma. [38] Firist wanda yake daga zuriyar Haruna zai raka
Lawiyawa sa’ad da suke karɓan zakka, Lawiyawan kuma za su kawo kashi ɗaya
bisa goma na zakka zuwa gidan Allahnmu, su kawo a ɗakunan ajiya na baitulmali.
[39] Mutanen Isra’ila haɗe da Lawiyawa, za su kawo sadakokinsu na hatsi, sabon
ruwan inabi da mai a ɗakunan ajiya inda ake ajiyar kayayyakin wuri mai tsarki
da kuma inda firistoci, matsaran ƙofofi da kuma mawaƙa suke zama.

“Ba za mu ƙyale gidan Allahnmu ba.”

# 11

*Sababbin mazaunan Urushalima*

[1] To, fa, shugabannin mutane suka zauna a Urushalima, sauran mutanen kuma
suka jefa ƙuri’a don su kawo mutum ɗaya daga kowane mutum goma don su zauna
a Urushalima, birni mai tsarki, yayinda sauran tara suka zauna a garuruwansu. [2] Sai
mutane suka yaba wa dukan mutanen da suka ba da kansu da yardar rai su zauna a
Urushalima.

[3] Waɗannan su ne shugabannin yankuna waɗanda suka zauna a Urushalima
(ko da yake waɗansu Isra’ilawa, da firistoci, da Lawiyawa, da ma’aikatan
haikali, da zuriyar bayin Solomon, suka yi zama a cikin garuruwan Yahuda,
kowanne a mallakarsa cikin garuruwa dabam-dabam, [4] yayinda sauran
mutane daga Yahuda da Benyamin suka zauna a Urushalima).

Daga zuriyar Yahuda akwai,

* **10:36** Ɗan fari na ’ya’yanmu maza. Dokar Allah. Dubi Fit 13.2,12-15; 34.19,20.

Atahiya ɗan Uzziya, ɗan Zakariya, ɗan Amariya, ɗan Shefatiya, ɗan Mahalalel, wani zuriyar Ferez;

5 da Ma’asehiya ɗan Baruk, ɗan Kol-Hoze, ɗan Hazahiya, ɗan Adahiya, ɗan Yohiyarib, ɗan Zakariya, zuriyar Shela.

6 Zuriyar Ferez waɗanda suka zauna a Urushalima sun kai ɗari huɗu da sittin da takwas, dukansu kuwa muhimman mutane ne.

7 Daga zuriyar Benyamin akwai,

Sallu ɗan Meshullam, ɗan Yowed, ɗan Fedahiya, ɗan Kolahiya, ɗan Ma’asehiya, ɗan Itiyel, ɗan Yeshahiya,
8 da mabiyansa, Gabbai da Sallai, mutum 928.

9 Yowel ɗan Zikri ne babban shugabansu, Yahuda kuma ɗan Hassenuwa, ya shugabanci Yanki na Biyu na birni.

10 Daga firistoci akwai,

Yedahiya ɗan Yohiyarib, da Yakin,

11 da Serahiya ɗan Hilkiya, ɗan Meshullam, ɗan Zadok, ɗan Merahiyot, ɗan Ahitub, mai lura da abubuwa a cikin gidan Allah,
12 tare da ’yan’uwansu waɗanda suke aiki domin haikali, su 822 ne.

Akwai kuma Adahiya ɗan Yeroham, ɗan Felaliya, ɗan Amzi, ɗan Zakariya, ɗan Fashhur, ɗan Malkiya,
13 da ’yan’uwansa waɗanda suke shugabannin iyalai, su 242.

Sai kuma Amashsai ɗan Azarel, ɗan Ahzai, ɗan Meshillemot, ɗan Immer,
14 da ’yan’uwansa, su 128 ne muhimman mutane.

Babban shugabansu shi ne Zabdiyel ɗan Haggedolim.

15 Daga Lawiyawa kuwa akwai,

Shemahiya ɗan Hasshub, ɗan Azrikam, ɗan Hashabiya, ɗan Bunni,

16 da Shabbetai, da kuma Yozabad, biyu cikin shugabanni Lawiyawa waɗanda suke da nawayar aiki waje da gidan Allah.

17 Sai kuma Mattaniya ɗan Mika, ɗan Zabdi, ɗan Asaf, shugaban da yake bi da hidimar godiya da kuma addu’a.

Sai Bakbukiya, na biyu a cikin ’yan’uwansa;

da Abda ɗan Shammuwa, ɗan Galal, ɗan Yedutun.

18 Lawiyawan da suke cikin birni mai tsarki sun kai 284.

19 Matsaran ƙofofi kuwa su ne,

Akkub, da Talmon, da ’yan’uwansu waɗanda suke tsaron ƙofofi, su 172 ne.

20 Sauran Isra’ilawa tare da firistoci, da Lawiyawa sun kasance a dukan garuruwan Yahuda, kowanne a mallakar kakansa.

21 Ma’aikatan haikali sun zauna a kan tudun Ofel. Ziha, da Gishfa ne suke lura da su.

22 Babban shugaban Lawiyawa a Urushalima shi ne Uzzi ɗan Bani, ɗan Hashabiya, ɗan Mattaniya, ɗan Mika. Uzzi yana ɗaya daga zuriyar Asaf, waɗanda suke mawaƙan da suke da nawayar hidima a gidan Allah.
23 Mawaƙa sun bi umarnan sarki, a kan abin da za su yi kowace rana.

24 Fetahahiya ɗan Meshezabel, ɗaya daga zuriyar Zera ɗan Yahuda ne, wakilin sarki cikin dukan al’amuran da suka shafi mutane.

25 Game da ƙauyukan da filayensu, waɗansu mutanen Yahuda suka zauna a Kiriyat Arba da ƙauyukanta, da Dibon da ƙauyukanta, da Yekabzeyel da ƙauyukanta.
26 Akwai su kuma a Yeshuwa, da Molada, da Bet-Felet,
27 da Hazar Shuwal, da Beyersheba da ƙauyukanta.
28 Akwai su a Ziklag, da Mekona da ƙauyukanta.
29 Suna nan kuma a En Rimmon, da Zora, da Yarmut,
30 da Zanowa, da Adullam da ƙauyukansu, da Lakish da gonakinta, da kuma Azeka da ƙauyukanta. Saboda haka sun yi zama tun daga Beyersheba har zuwa Kwarin Hinnom.

31 Zuriyar mutanen Benyamin daga Geba sun zauna a Mikmash, da Aiya, da Betel
da ƙauyukanta, 32 da Anatot, da Nob, da Ananiya, 33 da Hazor, da Rama, da Gittayim,
34 da Hadid, da Zeboyim, da Neballat, 35 da Lod, da Ono, da kuma a Kwarin Masu
sana'a.
36 Waɗansu gundumomin Lawiyawan Yahuda sun zauna a Benyamin.

# 12

*Firistoci da Lawiyawa*

1 Waɗannan su ne firistoci da Lawiyawa waɗanda suka komo tare da Zerubbabel ɗan Sheyaltiyel da kuma Yeshuwa.

Serahiya, Irmiya, Ezra,
2 Amariya, Malluk, Hattush
3 Shekaniya, Rehum, Meremot,
4 Iddo, Ginneton, Abiya,
5 Miyamin, Mowadiya, Bilga,
6 Shemahiya, Yohiyarib, Yedahiya,
7 Sallu, Amok, Hilkiya da Yedahiya.

Waɗannan su ne shugabannin firistoci da 'yan'uwansu a kwanakin Yeshuwa.

8 Lawiyawan su ne Yeshuwa, Binnuyi, Kadmiyel, Sherebiya, Yahuda, da kuma
Mattaniya, wanda tare da 'yan'uwansa yake lura da waƙoƙin godiya. 9 Bakbukiya
da Unni, 'yan'uwansu sun tsaya ɗaura da su a hidimomi.

10 Yeshuwa ne mahaifin Yohiyakim,
Yohiyakim shi ne mahaifin Eliyashib,
Eliyashib shi ne mahaifin Yohiyada,
11 Yohiyada shi ne mahaifin Yonatan,
Yonatan kuma mahaifin Yadduwa.

12 A kwanakin Yohiyakim, waɗannan su ne shugabannin iyalan firistoci,

na iyalin Serahiya, Merahiya;
na iyalin Irmiya, Hananiya;
13 na iyalin Ezra, Meshullam;
na iyalin Amariya, Yehohanan;
14 na iyalin Malluk, Yonatan;
na iyalin Shebaniya, Yusuf;
15 na iyalin Harim, Adna;
na iyalin Merahiyot, Helkai;
16 na iyalin Iddo, Zakariya;
na iyalin Ginneton, Meshullam;
17 na iyalin Abiya, Zikri;
na iyalin Miniyamin da na Mowadiya, Filtai;
18 na iyalin Bilga, Shammuwa;
na iyalin Shemahiya, Yehonatan;
19 na iyalin Yohiyarib, Mattenai;
na iyalin Yedahiya, Uzzi;

20 na iyalin Sallu, Kallai;
na iyalin Amok, Eber;
21 na iyalin Hilkiya, Hashabiya;
na iyalin Yedahiya, Netanel.

22 Shugabannin iyalin Lawiyawa a kwanakin Eliyashib, Yohiyada, Yohanan da
Yadduwa, da kuma na firistoci, an rubuta su a zamanin mulkin Dariyus mutumin
Farisa. 23 Shugabannin iyali cikin zuriyar Lawi har zuwa lokacin Yohanan ɗan
Eliyashib, an rubuta su a cikin littafin tarihi. 24 Shugabannin Lawiyawa kuwa su
ne Hashabiya, Sherebiya, Yeshuwa ɗan Kadmiyel, da ’yan’uwansu, waɗanda suka
tsaya ɗaura da su don su yi yabo da kuma godiya, sashe ɗaya kan ba da amsa ga
ɗaya sashen, kamar yadda Dawuda mutumin Allah ya umarta.
25 Mattaniya, Bakbukiya, Obadiya, Meshullam, Talmon da Akkub su ne matsaran
ƙofofi waɗanda suka yi tsaron ɗaukan ajiya a ƙofofi. 26 Sun yi hidima a kwanakin
Yohiyakim ɗan Yeshuwa, ɗan Yozadak, kuma a kwanakin Nehemiya gwamna da
kuma na Ezra firist da kuma marubuci.

### *Keɓewar katangar Urushalima*

27 A keɓewar katangar Urushalima, an nemi Lawiyawa daga inda suke zama aka
kawo su Urushalima don su yi bikin miƙawa da farin ciki da waƙoƙin godiya da
kuma kiɗin kuge, garaya da molo. 28 Aka kuma tattara mawaƙa su ma daga yankin
kewayen Urushalima, daga ƙauyukan Netofawa, 29 daga Bet-Gilgal, da kuma daga
wuraren Geba da Azmawet, gama mawaƙan sun gina wa kansu ƙauyuka kewaye da
Urushalima.
30 Sa’ad da firistoci da Lawiyawa suka tsarkake kansu da tsarki, sai suka tsarkake
mutane, ƙofofi da kuma katanga.
31 Sai na sa shugabannin Yahuda suka haura zuwa bisan katangar. Na kuma
sa manyan ƙungiyoyi biyu na mawaƙa su miƙa godiya. Ɗaya ya haura zuwa
bisan katangar zuwa dama, wajen Kofar Juji. 32 Hoshahiya da rabin shugabannin
Yahuda kuwa suka bi su, 33 tare da Azariya, Ezra, Meshullam, 34 Yahuda, Benyamin,
Shemahiya, Irmiya, 35 da waɗansu firistoci kuma da ƙahoni, da kuma Zakariya ɗan
Yonatan, ɗan Shemahiya, ɗan Mattaniya, ɗan Mikahiya, ɗan Zakkur, ɗan Asaf, 36 da
’yan’uwansa, Shemahiya, Azarel, Milalai, Gilalai, Ma’ai, Netanel, Yahuda da Hanani,
tare da kayan kiɗi da Dawuda mutumin Allah ya umarta. Ezra malamin Doka ya
jagoranci jerin gwanon. 37 A Kofar Maɓuɓɓuga suka ci gaba kai tsaye suka haura
matakalan Birnin Dawuda a kan hawa zuwa katangar suka wuce a bisa gidan Dawuda
zuwa Kofar Ruwa wajen gabas.
38 Kungiyar mawaƙa ta biyu suka yi jerin gwano a ɗaya gefen. Na bi su a bisan
katangar, tare da rabin mutanen, muka wuce Hasumiya Tanderu zuwa Katanga Mai
Faɗi, 39 bisa Kofar Efraim, Kofar Yeshana, Kofar Kifi, Hasumiyar Hananel da kuma
Hasumiya ɗari, har zuwa Kofar Tumaki. A Kofar Matsara suka tsaya.
40 Kungiyoyin mawaƙa biyu da suka yi godiya suka ɗauki wurarensu a gidan Allah,
haka ma ni, tare da rabin shugabanni, 41 da kuma firistoci, Eliyakim, Ma’asehiya,
Miniyamin, Mikahiya, Eliyohenai, Zakariya da Hananiya tare da ƙahoninsu, 42 haka
ma Ma’asehiya, Shemahiya, Eleyazar, Uzzi, Yehohanan, Malkiya, Elam da Ezer.
Mawaƙan suka rera waƙoƙi a ƙarƙashin kulawar Yezrahiya. 43 A rana ta uku kuma
suka miƙa manyan hadayu, suna farin ciki domin Allah ya ba su farin ciki mai girma.
Mata da yara suka yi farin ciki su ma. An ji ƙarar farin ciki da ake yi a Urushalima
daga nesa.
44 A lokacin an naɗa mutane su lura da ɗakunan ajiya don sadakoki, nunan fari da
kuma zakka. Daga gonakin garuruwan da suke kewaye za su kawo sassan da Dokar

ta umarta zuwa ɗakunan ajiya domin firistoci da Lawiyawa, gama Yahuda ya ji daɗin
aikin firistoci da Lawiyawa. 45 Sun yi hidimar Allahnsu da kuma hidimar tsarkakewa,
kamar yadda mawaƙa da matsaran ƙofofi suka yi, bisa ga umarnin Dawuda da ɗansa
Solomon. 46 Gama tun dā, a kwanakin Dawuda da Asaf, akwai masu bi da mawaƙa da
kuma na waƙoƙin yabo da na godiya ga Allah. 47 Saboda haka a kwanakin Zerubbabel
da Nehemiya, dukan Isra'ila suka ba da sashe na kowace rana domin mawaƙa da
matsaran ƙofofi. Suka kuma keɓe sashe don sauran Lawiyawa, Lawiyawan kuma
suka keɓe sashe don zuriyar Haruna.

# 13

*Gyare-gyaren ƙarshe na Nehemiya*

1 A wannan rana aka karanta Littafin Musa da ƙarfi a kunnuwan mutane aka kuma
sami an rubuta cewa kada a karɓi mutumin Ammon ko mutumin Mowab cikin taron
Allah, 2 domin ba su taryi Isra'ila da abinci da ruwa ba amma suka yi hayar Bala'am
don yă kira la'ana a kansu. (Amma Allahnmu, ya mai da la'anar ta zama albarka.)
3 Sa'ad da mutane suka ji wannan doka, sai suka ware daga Isra'ila duk waɗanda
suke na baƙon zuriya.

4 Kafin wannan, an sa Eliyashib firist yă lura da ɗakuna ajiyar gidan Allahnmu.
Yana da dangantaka na kurkusa da Tobiya, 5 ya kuma tanada masa babban ɗakin
da dā ake ajiyar hadayun hatsi da turare da kayayyaki haikali, da kuma zakan hatsi,
sabon ruwan inabi da kuma mai da aka umarta don Lawiyawa, mawaƙa da kuma
matsaran ƙofofi, da kuma sadakoki domin firistoci.

6 Amma yayinda dukan wannan yake faruwa, ba ni a Urushalima, gama a shekara
ta talatin da biyu na Artazerzes sarkin Babilon na dawo wurin sarki. A wani lokaci
daga baya na nemi izininsa 7 sai na koma zuwa Urushalima. A nan na ji game da
mugun abin da Eliyashib ya aikata da ya tanada wa Tobiya ɗaki a filayen gidan
Allah. 8 Na ɓace rai ƙwarai na kuma zubar da dukan kayan gidan Tobiya daga ɗakin.
9 Na umarta a tsarkake ɗakunan, sa'an nan na mayar da kayan gidan Allah a cikin
ɗakunan, tare da hadayun hatsi da kuma turare.

10 Na kuma ji cewa sassan da ake ba wa Lawiyawa ba a ba su ba, cewa kuma
dukan Lawiyawa da mawaƙan da suke da hakkin hidima sun koma gonakinsu. 11 Sai
na tsawata wa shugabanni na kuma tambaye su na ce, "Me ya sa aka ƙyale gidan
Allah?" Sa'an nan na kira su gaba ɗaya na sa su a wuraren aikinsu.

12 Dukan Yahuda suka kawo zakan hatsi, sabon ruwan inabi da mai cikin ɗakunan
ajiya. 13 Na sa Shelemiya firist, Zadok marubuci, da wani Balawe mai suna Fedahiya
su lura da ɗakunan ajiya na kuma sa Hanan ɗan Zakkur, ɗan Mattaniya ya zama
mataimakinsu, domin an ɗauka waɗannan mutane amintattu ne. Aka ba su hakkin
raban kayayyaki wa 'yan'uwansu.

14 Ka tuna da ni saboda wannan, ya Allahna, kuma kada ka shafe abin da na yi da
aminci domin gidan Allahna da kuma hidimarsa.

15 A waɗannan kwanaki, na ga mutane a Yahuda suna matse ruwan inabi a
ranar Asabbaci suna kuma kawo hatsi suna labta su a kan jakuna, tare da ruwan
inabi, 'ya'yan inabi, ɓaure da kaya iri-iri. Suna kuma kawowa dukan wannan
cikin Urushalima a ranar Asabbaci. Saboda haka na gargaɗe su a kan sayar da
abinci a wannan rana. 16 Mutane daga Taya waɗanda suke zama a Urushalima suna
shigar da kifi da kaya iri-iri na 'yan kasuwa suna kuma sayar da su a Urushalima
a ranar Asabbaci wa mutanen Yahuda. 17 Sai na tsawata wa manyan Yahuda na ce
musu, "Wanda irin mugun abu ke nan kuke yi, kuna ƙazantar da ranar Asabbaci?

18 Kakanninku ba su yi irin waɗannan abubuwa ba, har Allahnmu ya kawo dukan
masifun nan a kanmu da kuma a kan wannan birni? Yanzu kuna tsokanar fushi mai
yawa a kan Isra'ila ta wurin ƙazantar da Asabbaci."
19 Sa'ad da inuwar yamma ya fāɗo a ƙofofin Urushalima kafin Asabbaci, na umarta
a rufe ƙofofi kuma kada a buɗe sai Asabbaci ya wuce. Na kafa waɗansu mutanena
a ƙofofin don kada a shigo da wani kaya a ranar Asabbaci. 20 Sau ɗaya ko biyu,
'yan kasuwa da masu sayar da kowane irin kaya suka kwana waje da Urushalima.
21 Amma na ja kunnensu na ce, "Me ya sa kuke kwana kusa da katanga? In kuka
ƙara yin haka, zan kama ku." Daga wannan lokaci har zuwa gaba ba su ƙara zuwa
a ranar Asabbaci ba. 22 Sai na umarci Lawiyawa su tsarkake kansu su kuma tafi su
yi tsaron ƙofofi don a kiyaye ranar Asabbaci da tsarki.

Ka tuna da ni saboda wannan shi ma, ya Allahna, ka nuna mini jinƙai bisa ga madawwamiyar ƙaunarka.

23 Ban da haka, a waɗannan kwanakin na ga mutanen Yahuda waɗanda suka auri
mata daga Ashdod, Ammon da Mowab. 24 Rabin 'ya'yansu suna yaren Ashdod ko
kuwa wani yare na waɗansu mutane, ba su kuwa san yadda za su yi Yahudanci
ba. 25 Na tsawata musu na kuma kira la'ana a kansu. Na bugi waɗansu mutane na
kuma ja gashin kansu. Na sa suka yi rantsuwa da sunan Allah na ce, "Kada ku ba
da 'ya'yanku mata aure ga 'ya'yansu maza, ba kuwa za ku auri 'ya'yansu mata wa
'ya'yanku maza ko wa kanku ba. 26 Ba don aure-aure irin waɗannan ne Solomon
sarkin Isra'ila ya yi zunubi ba? A cikin yawancin al'ummai babu sarki kamar sa.
Allahnsa ya ƙaunace shi, Allah kuma ya mai da shi sarki a kan dukan Isra'ila, amma
duk da haka baren mata suka rinjaye shi ga zunubi. 27 Yanzu za mu ji cewa ku ma
kuna yin duk wannan mugunta kuna zama marasa aminci ga Allahnmu ta wurin
auren baren mata?"
28 Ɗaya daga cikin 'ya'yan Yohiyada maza, ɗan Eliyashib babban firist, surukin
Sanballat mutumin Horon ne. Na kuwa kore shi daga wurina.

29 Ka tuna da su, ya Allahna, domin sun ƙazantar da aikin firist da kuma alkawarin
aikin firist da na Lawiyawa.

30 Saboda haka na tsarkake firistoci da Lawiyawa daga kowane baƙon abu, na
kuma ba su aikinsu, kowa ga aikinsa. 31 Na kuma yi tanadi don sadakokin itace
a ƙayyadaddun lokuta, da kuma don nunan fari.

Ka tuna da ni da alheri, ya Allahna.

# Esta

*An tumɓuke sarauniya Bashti*

[1] Ga abin da ya faru a zamanin Zerzes.* Zerzes ya yi mulki bisan larduna 127 daga
Indiya zuwa Kush. [2] A lokacin nan, Sarki Zerzes ya yi mulki daga gadon sarauta,
cikin mazaunin masarautar Shusha. [3] A shekara ta uku ta mulkinsa, ya yi wa dukan
hakimansa da ma'aikatansa liyafa. Shugabannin mayaƙan Farisa, da Mediya, da
yerimai; da kuma hakimai na lardunan suka kasance.

[4] Kwanaki 180 cif, ya nuna yawan dukiyar masarautarsa, da ɗaukakarta da kuma
darajar girmansa. [5] Sa'ad da waɗannan kwanaki suka wuce, sai sarki ya yi liyafa a
cikin lambun da aka shinge na fadar sarki wadda ta ɗauki kwana bakwai wa dukan
mutane daga ƙarami har zuwa babba, waɗanda suke zama a masarautar Shusha.
[6] Lambun yana da fararen labulen da aka rataye da shunayya na lallausan lilin, da
aka ɗaura da igiyoyin fararen lilin, da yadin jan garura, haɗe da zoban azurfa a kan
ginshiƙin farin ƙasa. A nan, akwai kujeru na zinariya da na azurfa a kan daɓe mai
ado da aka yi da duwatsu masu daraja, da farin ƙasa, da fararen duwatsun wuya,
da waɗansu duwatsu masu tsada. [7] Aka rarraba ruwan inabi cikin kwaf na zinariya,
kowanne kuwa dabam yake da ɗayan. Ruwan inabin kuwa yana da yawa, bisa ga
wadatar sarki. [8] Bisa ga umarnin sarki, aka bar kowane baƙo yǎ sha yadda ya ga
dama, gama sarki ya umarci dukan bayin da suke rarraba ruwan inabin su ba wa
kowa abin da yake so.

[9] Sarauniya Bashti ita ma ta yi liyafa saboda mata a fadar Sarki Zerzes.

[10] A rana ta bakwai, sa'ad da Sarki Zerzes, ya yi tilis da ruwan inabi, sai ya umarci
bābānni bakwai waɗanda suke yin masa hidima, wato, Mehuman, Bizta, Harbona,
Bigta, Abagta, Zetar da Karkas, [11] su kawo Sarauniya Bashti a gabansa, sanye da
rawanin sarautarta, don ta nuna kyanta wa mutane da kuma hakimai, gama ita
kyakkyawa ce ƙwarai. [12] Amma da masu hidima suka ba da umarnin sarki, sai
Sarauniya Bashti ta ƙi zuwa. Wannan ya ɓata wa sarki rai, ya kuma yi fushi ƙwarai.

[13] Da yake, al'ada ce sarki yǎ nemi shawara daga sanannu a batun doka da adalci,
sai ya yi magana da masu hikima waɗanda suke fahimtar lokuta [14] suke kuma mafi
kusa da sarki. Waɗannan masu hikima kuwa su ne, Karshena, Shetar, Admata,
Tarshish, Meres, Marsena da kuma Memukan. Su hakimai bakwai ne na Farisa
da Mediya waɗanda suke da dama ta musamman ta kaiwa ga sarki, suke kuma da
matsayi mafi girma a masarautar.

[15] Ya ce, "Bisa ga doka, me za a yi wa Sarauniya Bashti? Gama ta ƙi yin biyayya da
umarnin sarki Zerzes da bābānni suka kai mata?"

[16] Sai Memukan ya amsa a gaban sarki da hakimai ya ce, "Sarauniya Bashti ta yi
laifi, ba ga sarki kaɗai ba, amma ga dukan hakimai ma, da kuma mutanen dukan
lardunan sarki Zerzes. [17] Domin halin Sarauniya zai zama sananne ga dukan mata, ta
haka kuwa za su ƙasƙantar da mazansu su kuma ce, 'Sarki Zerzes ya umarta a kawo
Sarauniya Bashti a gabansa, amma ta ƙi zuwa.' [18] Wannan rana matan hakiman
Farisa da na Mediya waɗanda suka ji game da halin sarauniya, za su yi haka wa
dukan hakiman sarki. Zai zama babu ƙarshen rashin bangirma da kuma reni.

[19] "Saboda haka, in ya gamshi sarki, bari yǎ ba da hatimi na sarauta, bari kuma a
rubuta shi cikin dokokin Farisa da Mediya, wanda ba za a iya sokewa ba, cewa Bashti
ba za tǎ ƙara zuwa gaban sarkin Zerzes ba. Bari kuma sarki yǎ ba da matsayinta na

* **1:1** Da Ibraniyanci Ahasuwerus; a nan da kuma a dukan littafin Esta.

sarauta ga wata, wadda ta fi ta. 20 Ta haka, sa'ad da aka yi shelar dokar sarki ko'ina a
fāɗin masarautarsa, dukan mata za su ba wa mazansu girma, daga ƙarami har zuwa
babba."
21 Sarki da hakimansa suka gamsu da wannan shawara. Saboda haka sarki ya
yi kamar yadda Memukan ya faɗa. 22 Ya aika da saƙo zuwa ga dukan ɓangarorin
masarautar, zuwa ga kowane lardi a irin nasa rubutu, zuwa kuma ga kowane mutane
a nasu harshe, ana shelar a kowane yare na mutane, cewa kowane mutum yǎ zama
mai mulki bisa gidansa.

# 2

*An mai da Esta sarauniya*

1 Daga baya sa'ad da fushin Sarki Zerzes ya huce, sai ya tuna da Bashti da abin da ta
yi, da kuma dokar da ya bayar game da ita. 2 Sai masu hidimar sarki na musamman,
suka kawo shawara cewa, "Bari a nemi, kyawawan budurwai saboda sarki. 3 Bari
sarki yǎ naɗa komishinoni a kowane yanki na masarautarsa, domin su kawo dukan
waɗannan kyawawan 'yan mata cikin harabar mazaunin masarautar a Shusha. Bari
a sa su a hannun Hegai, bābān sarki, wanda yake lura da mata, bari kuma a yi
musu kulawa ta musamman. 4 Sa'an nan bari yarinyar da ta gamshi sarki, tǎ zama
sarauniya a maimakon Bashti." Wannan shawara ta gamshi sarki, ya kuwa yi na'am
da ita.
5 To, a cikin mazaunin masarauta a Shusha, akwai wani mutumin Yahuda, daga
Kabilar Benyamin mai suna Mordekai, ɗan Yayir, ɗan Shimeyi, ɗan Kish, 6 wanda
Nebukadnezzar sarkin Babilon ya ɗauka tare 'yan zaman bauta cikin waɗanda ya
ɗauko daga Urushalima, tare da Yekoniya, sarkin Yahuda. 7 Mordekai yana da wata
'yar kawunsa mai suna Hadassa, wanda ya yi reno, ba ta da mahaifi ko mahaifiya.
Ita ce yarinyar da aka santa da suna Esta. Kyakkyawa ce ƙwarai. Mordekai dai ya
ɗauke ta tamƙar 'yarsa sa'ad da mahaifinta da mahaifiyarta suka mutu.
8 Da aka yi shelar umarni da dokar sarki, sai aka kawo 'yan mata masu yawa
a mazaunin masarauta a Shusha, aka kuma sa su ƙarƙashin kulawar Hegai. Aka
kawo Esta ma zuwa fadar sarki, aka danƙa ta wa Hegai, wanda yake lura da mata.
9 Yarinyar ta gamshe shi, ta kuma sami tagomashinsa. Nan da nan ya tanada mata,
ya ba ta man shafawa da abinci na musamman. Ya ba ta bayi mata bakwai da aka
zaɓa daga fadar sarki. Ya kuma kai ta tare da bayinta zuwa wuri mafi kyau na gidan
matan kulle.
10 Esta ba tǎ bayyana asalin al'ummarta da na iyalinta ba, domin Mordekai ya hana
yin haka. 11 Kowace rana Mordekai yana kai da komowa kusa da harabar filin gidan
matan kulle, domin ya san yadda Esta take, da kuma abin da yake faruwa da ita.
12 Kafin a kai kowace yarinya wurin Sarki Zerzes, sai ta gama watanni goma sha
biyu cif ana yin mata kwalliyar da aka tsara, akan ɗauki watanni shida ana shafa
mata man mur, a ɗauki watanni shida kuma ana shafa mata man ƙanshi da kayan
shafe-shafe. 13 A kuma koya mata yadda za tǎ tafi wurin sarki. Aka ba ta duk abin
da take so ta riƙe daga gidan matan kulle zuwa fadar sarki. 14 Da yamma za tǎ tafi
can, da safe kuma ta dawo wani ɓangaren gidan matan kullen da yake a ƙarƙashin
kulawar Sha'ashgaz, bābā na sarki, wanda yake lura da ƙwarƙwarai. Ba ta dawowa
wurin sarki sai in ta gamshe shi, sai ya kuma kira ta da suna.
15 Sa'ad da lokaci ya yi da Esta (yarinyar da Mordekai ya ɗauka tamƙar 'yarsa, 'yar
kawunsa Abihayil) za tǎ shiga wurin sarki, ba tǎ nemi a ba ta kome ba in ban da abin
da Hegai, bābān sarki mai lura da gidan matan kulle, ya ba da shawara. Esta kuwa
ta sami tagomashin kowa da ya ganta. 16 Aka kai Esta wurin Sarki Zerzes a mazaunin
sarauta a wata na goma, watan Tebet, a shekara ta bakwai ta mulkinsa.

[17] To, sarki ya so Esta fiye da duk sauran matan, ta kuma sami tagomashinsa
da kuma yardarsa fiye da duk sauran budurwai. Saboda haka ya sa rawanin
sarauta a kanta, ya kuma mai da ita sarauniya a maimakon Bashti. [18] Sarki
kuwa ya yi ƙasaitacciyar liyafa, liyafar Esta, wa dukan hakimansa da shugabannin
masarautarsa. Ya yi shelar hutu ko'ina a larduna, ya kuma raba kyautai a yalwace
irin na sarauta.

### *Mordekai ya gano maƙarƙashiya*

[19] Sa'ad da aka tara budurwai karo na biyu, Mordekai kuwa yana zama a bakin
ƙofar sarki. [20] Amma Esta ta ɓoye asalin iyalinta da na al'ummarta yadda Mordekai
ya ce ta yi, gama ta ci gaba da bin umarnan Mordekai yadda take yi sa'ad da yake
renonta.
[21] Sa'ad da Mordekai yake zaune a bakin ƙofar sarki, sai Bigtana da Teresh, biyu
daga cikin hafsoshin sarki masu gadin ƙofar shiga, suka yi fushi, suka kuma ƙulla su
kashe sarki Zerzes. [22] Mordekai kuwa ya sami labarin makircin, ya kuma faɗa wa
Sarauniya Esta, wadda ta faɗa wa sarki, ta kuma nuna masa cewa Mordekai ne ya
ji. [23] Sa'ad da aka bincika labarin aka kuma iske gaskiya ne, sai aka rataye hafsoshin
nan biyu a wurin rataye mai laifi. Aka rubuta dukan wannan a cikin littafin tarihi a
gaban sarki.

# 3

### *Makircin Haman na neman yă hallaka Yahudawa*

[1] Bayan waɗannan al'amura, sai Sarki Zerzes ya girmama Haman ɗan Hammedata,
mutumin Agag, ya ɗaukaka shi, ya kuma ba shi matsayi mafi girma fiye da na dukan
sauran hakiman. [2] Dukan masu hidimar da suke a ƙofar sarki suka riƙa durƙusa suna
ba wa Haman girma, gama sarki ya ba da umarni a yi masa haka. Amma Mordekai
bai durƙusa ya ba shi girma ba.
[3] Sa'an nan masu hidimar da suke a ƙofar sarki suka tambaye Mordekai, "Me ya
sa ba ka yin biyayya da umarnin sarki?" [4] Kowace rana suna masa magana, amma
ya ƙi yă yi. Saboda haka, suka faɗa wa Haman game da wannan don su ga ko za a
jure da halin Mordekai, gama ya faɗa musu cewa shi mutumin Yahuda ne.
[5] Sa'ad da Haman ya ga cewa Mordekai ba ya durƙusa ko yă girmama shi, sai ya
fusata. [6] Da yake an faɗa masa asalin Mordekai, sai ya ga a kashe Mordekai kaɗai ba
zai biya masa bukata ba. A maimakon haka, Haman ya nemi hanya a hallaka dukan
mutanen Mordekai, wato, Yahudawa, a ko'ina a dukan masarautar Zerzes.
[7] A shekara ta goma sha biyu ta Sarki Zerzes, a wata na farko, watan Nisan, sai
suka jefa *fur* (wato, ƙuri'a) a gaban Haman don a zaɓi rana da watan da zai dace da
ƙulle-ƙullen. Sai ƙuri'a ta fāɗa a kan wata na goma sha biyu, wato, watan Adar.
[8] Sai Haman ya ce wa Sarki Zerzes, "Akwai waɗansu mutanen da suke a warwatse,
sun kuma bazu a cikin mutane cikin dukan lardunan masarautarka, waɗanda
al'adunsu sun yi dabam da na dukan sauran mutane. Mutanen nan ba sa biyayya
da dokokin sarki; ba zai yi wa sarki kyau a jure su ba. [9] In ya gamshi sarki, bari a
yi doka, don a hallaka su, zan kuma sa talenti dubu goma na azurfa a cikin ma'ajin
fada saboda mutanen da suka aikata wannan sha'ani."
[10] Saboda haka sarki ya zare zoben hatimi daga yatsarsa, ya ba wa Haman ɗan
Hammedata, mutumin Agag, abokin gāban Yahudawa. [11] Sarki ya ce wa Haman, "Ka
riƙe kuɗin, ka kuma yi da mutanen yadda ka ga dama."
[12] Sa'an nan aka kira magatakardun sarki a rana ta goma sha uku na wata na fari.
Suka rubuta dukan umarnin Haman a irin rubutun kowane lardi, kuma cikin harshen
kowane mutane, zuwa ga shugabannin mahukuntai na sarki, da gwamnonin larduna
dabam-dabam, da kuma hakiman mutane dabam-dabam. Aka rubuta waɗannan a

sunan Sarki Zerzes da kansa, aka kuma hatimce da zobensa. 13 Aka aika ’yan-kada-
tă-kwana da saƙoni zuwa dukan lardunan sarki da umarni a hallaka, a karkashe, a
kuma kawar da dukan Yahudawa, manya da ƙanana, mata da yara, a kuma washe
kayayyakinsu. 14 Za a ba da kofin rubutun a matsayin doka a kowane lardi, a kuma
sanar da mutanen kowace al’umma, domin su zauna da shiri don wannan rana.
15 Bisa ga umarnin sarki, sai ’yan-kada-tă-kwana, suka tafi da sauri. Aka ba da
umarni a mazaunin masarauta da yake a Shusha. Sai Sarki da Haman suka zauna
don su sha, amma birnin Shusha ya ruɗe.

# 4

*Mordekai ya lallashi Esta ta taimaka*

1 Sa’ad da Mordekai ya sami labari game da dukan abin da aka yi, sai ya yayyage
rigunansa, ya sanya tsummokin makoki, ya zuba toka a kā, ya kuma shiga ciki birni
yana kuka mai zafi da ƙarfi. 2 Amma ya kai bakin ƙofar sarki ne kawai, gama ba
a yarda wani sanye da tsummokin makoki yă shiga cikin birni ba. 3 Aka yi makoki
sosai da azumi, da kuka mai zafi a cikin Yahudawa a kowane lardin da aka kai doka
da kuma umarnin sarki. Mutane da yawa suka kwanta a cikin tsummokin makoki
da kuma toka.
4 Sa’ad da bayi da bābānnin Esta suka zo suka faɗa mata game da Mordekai, sai ta
damu ƙwarai. Ta aika masa da riguna domin yă sa a maimakon tsummokin makoki,
amma ya ƙi. 5 Sai Esta ta kira Hatak, ɗaya daga cikin bābānnin sarkin da aka ba shi
aikin lura da ita, ta umarce shi yă yi tambaya me ke damun Mordekai da kuma me
ya jawo haka.
6 Saboda haka Hatak ya tafi wurin Mordekai a dandalin birni, a gaban ƙofar sarki.
7 Mordekai ya faɗa masa duk abin da ya faru da shi, haɗe da yawan kuɗin da Haman
ya yi alkawari zai zuba a ma’ajin fada don a hallaka Yahudawa. 8 Ya kuma ba shi
kofi na rubutaccen doka na kakkaɓe su, wanda aka wallafa a Shusha don yă nuna
wa Esta, yă bayyana mata. Mordekai ya faɗa wa Hatak yă iza ta tă tafi gaban sarki
domin tă yi roƙo don jinƙai, tă kuma roƙe shi saboda mutanenta.
9 Hatak ya koma ya ba wa Esta rahoton abin da Mordekai ya faɗa. 10 Sa’an nan Esta
ta umarce Hatak yă ce wa Mordekai, 11 “Dukan hafsoshin sarki da mutanen lardunan
sarki sun san cewa duk wanda ya tafi wurin sarki a shirayi na ciki, mace ko namiji,
ba tare da an kira shi ba, doka ɗaya ce take kan mutum, wato, kisa. Abu guda kawai
da ya sha bamban shi ne sai wanda sarki ya miƙa wa sandan sarauta na zinariya
don yă rayu. Kwana talatin ke nan ba a kira ni in tafi wurin sarki ba.”
12 Sa’ad da aka kai wa Mordekai rahoton maganan Esta, 13 sai ya mayar da wannan
amsa wa Esta cewa, “Kada ki yi tsammani cewa don kina a cikin gidan sarki, ke kaɗai
cikin dukan Yahudawa za ki tsira. 14 Gama in kin yi shiru a wannan lokaci, taimako
da ceto zai zo daga wani wuri saboda Yahudawa, amma ke da gidanki za ku hallaka.
Wa ya san ko saboda irin wannan lokaci ne kika sami wannan muƙami?”
15 Sai Esta ta aika da wannan amsa ga Mordekai cewa, 16 “Ka tafi, ka tattara dukan
Yahudawan da suke Shusha, ku yi azumi saboda ni. Kada ku ci ko ku sha, dare da
rana har kwana uku. Ni kuwa da bayina za mu yi azumi yadda kuke yi. Idan aka yi
haka, zan tafi wurin sarki, ko da yake wannan karya doka ce. Idan na hallaka, to, na
hallaka.”
17 Saboda haka, Mordekai ya tafi, ya aikata dukan umarnan Esta.

# 5

*Roƙon Esta ga sarki*

1 A rana ta uku, Esta ta sanya rigunanta na sarauta, ta tafi ta tsaya a harabar fada, a
gaban zaure sarki. Sarki yana zaune a kan gadon sarautarsa a zauren, yana fuskantar
ƙofar shiga. 2 Sa'ad da ya ga Sarauniya Esta tsaye a harabar, sai ya ji daɗin ganinta,
ya miƙa mata sandan sarauta na zinariya da take hannunsa. Sai Esta ta matsa kusa
ta taɓa kan sandan.
3 Sai sarki ya ce mata, "Me kike so, Sarauniya Esta? Mene ne roƙonki? Kai, ko
rabin masarautata ce, za a ba ki."
4 Esta ta ce, "In ya gamshi sarki, bari sarki, tare da Haman su zo wurin liyafar da
na shirya wa sarki yau."
5 Sai sarki ya ce, "Maza a kawo Haman don mu yi abin da Esta ta roƙa."
Saboda haka, sarki da Haman suka tafi liyafar da Esta ta shirya. 6 Yayinda suke
shan ruwan inabi, sarki ya sāke ce wa Esta, "Yanzu, mece ce bukatarki? Za a biya
miki shi. Kuma mene ne roƙonki? Kai, ko rabin masarautata ce, za a ba ki."
7 Esta ta amsa ta ce, "Bukatata da kuma roƙona shi ne, 8 in na sami tagomashi a
wurin sarki, in kuma sarki ya yarda yǎ biya mini bukatata, yǎ kuma ji roƙona, bari
sarki da Haman su zo gobe wurin liyafar da zan shirya musu. Sa'an nan zan amsa
tambayar sarki."

### *Fushin Haman a kan Mordekai*

9 Haman ya fita a ranan da murna, ya kuma ji daɗi. Amma sa'ad da ya ga Mordekai
a bakin ƙofar sarki, ya kuma lura cewa bai tashi, ko yǎ nuna bangirma a gabansa ba,
sai ya cika da fushi. 10 Duk da haka, Haman ya cije, ya tafi gida.
Sai ya kira abokansa da kuma matarsa, Zeresh, 11 ya yi ta taƙama game da ɗumbun
wadatarsa, da yawan 'ya'yansa maza, da dukan yadda sarki ya girmama shi, ya kuma
ɗaga shi bisan sauran hakimai da shugabanni. 12 Haman ya ƙara da cewa, "Ba duka
ke nan ba, kai, ni ne kaɗai mutumin da Sarauniya Esta ta gayyata yǎ tafi tare da sarki
zuwa liyafar da ta shirya. Ta sāke gayyace ni tare da sarki gobe. 13 Amma dukan
wannan bai biya mini bukata ba, muddin ina ganin wannan mutumin Yahudan nan
Mordekai, yana zama a bakin ƙofar sarki."
14 Matarsa Zeresh, da dukan abokansa suka ce masa, "Ka sa a gina wurin rataye mai
laifi, mai tsawo, ƙafa saba'in da biyar, da safe kuwa ka ce wa sarki a rataye Mordekai a
kansa. Sa'an nan ka tafi cin abincin dare tare da sarki da murna." Wannan shawarar
ta faranta wa Haman rai, ya kuma sa aka gina wurin rataye mai laifi.

## 6

### *An girmama Mordekai*

1 A daren nan, sarki bai iya barci ba, saboda haka ya ba da umarni a kawo, a kuma
karanta masa littafin tarihi na shekara-shekara, da rubutaccen labarin mulkinsa.
2 Aka tarar, a rubuce a ciki, cewa Mordekai ya tone ƙulle-ƙullen Bigtana da Teresh,
biyu daga hafsoshin sarki, waɗanda suke tsaron mashigin ƙofa, waɗanda suka ƙulla
su kashe Sarki Zerzes.
3 Sarki ya ce, "Wace girma da daraja ce aka ba wa Mordekai saboda wannan?"
Masu hidimarsa suka ce, "Ba a yi masa wani abu ba."
4 Sarki ya ce, "Wa yake a haraba?" Daidai lokacin kuwa Haman ya shigo harabar
waje na fada don yǎ yi magana da sarki a kan a rataye Mordekai a wurin rataye mai
laifin da ya shirya.
5 Masu yi wa sarki hidima, suka amsa, "Haman yana tsaye a haraba."
Sarki ya umarta, "A kawo shi ciki."
6 Sa'an nan Haman ya shigo, sai sarki ya ce masa, "Me ya kamata a yi wa mutumin
da sarki yake jin daɗi yǎ girmama?"

Haman dai ya yi tunani a ransa ya ce, “Wane ne sarki zai girmama in ba ni ba?”
7 Sai ya amsa wa sarki cewa, “Saboda mutumin da sarki yake jin daɗi yă girmama,
8 bari a kawo rigar sarautar da sarki ya taɓa sawa, da kuma dokin da sarki ya taɓa
hawa, wanda aka sa kambin sarauta a kai. 9 Sa’an nan, bari a ba da rigar da kuma
dokin wa ɗaya daga cikin manyan sarakuna mafi kirki na sarki. Bari shi kuma yă
sa wannan riga wa mutumin da sarki yake jin daɗi yă girmama, a kuma bi da shi
a bisan doki ko’ina a titunan birni, ana shela a gabansa ana cewa, ‘Wannan shi ne
abin da ake yin wa mutumin da sarki yake jin daɗi yă girmama!’ ”

10 Sarki ya umarci Haman ya ce, “Tafi yanzu ka karɓi rigar da dokin, ka kuma yi
yadda ka shawarta wa Mordekai, mutumin Yahudan nan, wanda yake zama a bakin
ƙofar sarki. Kada ka kāsa yin kome daga cikin abin da ka faɗa.”

11 Saboda haka, Haman ya karɓo rigar da dokin. Ya sa wa Mordekai rigar, ya
kuma bi da shi a kan doki ko’ina a titunan birnin, yana shela a gabansa yana cewa,
“Wannan shi ne abin da ake yi wa mutumin da sarki yake jin daɗi yă girmama!”

12 Daga baya, Mordekai ya dawo zuwa ƙofar sarki. Amma Haman ya ruga gida,
kansa a rufe, saboda baƙin ciki. 13 Ya je ya faɗa wa matarsa Zeresh, da dukan
abokansa, me ya same shi.

Masu ba shi shawara, da matarsa Zeresh, suka ce masa, “Idan Mordekai, wanda
ka fara fāɗuwa a gabansa, daga zuriyar Yahudawa yake, to, ba za ka yi nasara a
kansa ba, tabbatacce za ka fāɗi a gabansa!” 14 Suna cikin magana da shi ke nan, sai
ga bābānnin sarki, suka iso suka kuma hanzarta da Haman zuwa liyafar da Esta ta
shirya.

# 7

*An rataye Haman*

1 Saboda haka sarki da Haman suka tafi cin abinci wurin sarauniya Esta. 2 Yayinda
suke shan ruwan inabi a rana ta biyun nan, sai sarki ya sāke tambaya, “Sarauniya
Esta, me kike so? Za a ba ki. Mene ne roƙonki? Ko da rabin masarautata ne, za a ba
ki.”

3 Sai Sarauniya Esta ta amsa ta ce, “In na sami tagomashi a wurinka, ya sarki, in
kuma mai girma ya yarda, a bar ni da raina, wannan shi ne roƙona. Ka kuma sa
kada a kashe mutanena, wannan ita ce bukata. 4 Gama an sayar da ni da mutanena
don a hallaka, a karkashe mu, a kuma ƙi mu. Da a ce an sayar da mu kamar bayi
maza da mata ne, da na yi shiru, domin wannan zai zama abin da bai taka kara ya
karye ba, har da za a dami sarki a kai.”*

5 Sarki Zerzes ya tambayi Sarauniya Esta ya ce, “Wane ne shi? Ina mutumin da ya
yi ƙarfin halin yin wannan karambani?”

6 Esta ta ce, “Maƙiyi da abokin gāban, shi ne wannan mugun Haman.”

Sai Haman ya tsorota a gaban sarki da sarauniya. 7 Sarki ya tashi cikin fushi, ya
bar ruwan inabinsa, ya fita zuwa cikin lambun fada. Amma da Haman ya gane cewa
sarki ya riga ya yanke shawara a kan ƙaddararsa, ya dakata domin yă roƙi sarauniya
Esta saboda ransa.

8 Sarki yana dawowa daga lambun fada zuwa babban zauren liyafan ke nan, sai
ga Haman ya fāɗi a kan shimfiɗar da Esta take zaune.

Sarki ya tā da murya da ƙarfi ya ce, “Har ma zai ci mutuncin sarauniya yayinda
take tare da ni a cikin gida?”

Sarki bai ma rufe baki ba, sai bayin sarki suka rufe fuskar Haman. 9 Sai Harbona,
ɗaya daga cikin bābānni masu yi wa sarki hidima ya ce, “Akwai wurin rataye mai

* **7:4** Ko kuwa tabbatacce, gama ladar da abokin gābanmu zai bayar ba za a kwatanta da hasarar da sarki zai yi ba

laifi da tsayinsa ya kai ƙafa saba'in da biyar† yana nan tsaye kusa da gidan Haman.
Ya gyara shi ne domin a rataye Mordekai, wanda ya yi cece sarki wanda ya tone
makircin masu niyya su hallaka sarki."
Sai sarki ya ce, "Ku rataye shi a kansa!" 10 Saboda haka suka rataye Haman a kan
wurin rataye mai laifin da shi Haman ya shirya saboda Mordekai. Sa'an nan sarki
ya huce.

# 8

*Dokar sarki a madadin Yahudawa*

1 A wannan rana, Sarki Zerzes ya ba wa Esta mallakar Haman, abokin gāban
Yahudawa. Mordekai kuma ya zo gaban sarki, gama Esta ta faɗa yadda ta haɗa
dangi da shi. 2 Sarki ya cire zobensa na hatimi, wanda ya karɓo daga Haman ya ba
Mordekai. Esta kuma ta naɗa shi a kan mallakar Haman.
3 Esta ta sāke roƙon sarki, ta fāɗi a ƙafafunsa tana kuka. Ta roƙe shi yǎ kawo
ƙarshen mugun shirin nan na Haman, mutumin Agag; wanda ya shirya a kan
Yahudawa. 4 Sai sarki ya miƙa wa Esta sandan sarauta na zinariya, ta kuwa tashi
ta tsaya a gabansa.
5 Ta ce, "In sarki ya yarda, in kuma na sami tagomashi daga gare shi, idan kuma
ya gamshe shi yǎ yi abin da yake daidai, idan yana jin daɗina, bari a rubuta umarni
a soke hukuncin saƙonin da Haman ɗan Hammedata, mutumin Agag, ya shirya ya
kuma rubuta domin a hallaka Yahudawa a dukan lardunan sarki. 6 Gama yaya zan
jure da ganin masifa ta faɗa a kan mutanena? Yaya zan jure in ga an hallaka iyalina?"
7 Sarki Zerzes ya amsa wa Esta da Mordekai mutumin Yahuda, "Domin Haman ya
kai wa Yahudawa hari, na ba da mallakarsa ga Esta, an kuma rataye shi a wurin
rataye mai laifi. 8 Yanzu ku rubuta wata doka, a sunan sarki, a madadin Yahudawa,
yadda kuka ga ya fi kyau ku kuma hatimce ta da zoben hatimin sarki, gama babu
takardar da aka rubuta da sunan sarki, aka kuma hatimce da zobensa da za a iya
sokewa."
9 Nan da nan aka kira magatakardun fada, a ranar ashirin da uku ga watan uku,
wato, watan Siban. Suka rubuta dukan umarnan Mordekai ga Yahudawa, da kuma
ga shugabanni, da gwamnoni, da hakiman larduna 127 tun daga Indiya har zuwa
Kush. Aka rubuta waɗannan umarnan a rubutun kowane lardi, da kuma cikin
harshen kowane mutane. Aka kuma rubuta ga Yahudawa a rubutunsu da harshensu.
10 Mordekai ya yi rubutu da sunan Sarki Zerzes, ya hatimce saƙonin da zoben hatimin
sarki, ya kuma aika da su ta hannun masu 'yan aika a kan dawakai, waɗanda sukan
hau dawakai masu gudu sosai, da aka yi kiwonsu musamman saboda sarki.
11 Dokar sarki ta ba wa Yahudawa a kowace birni izini su taru, su kuma kāre kansu,
domin su hallaka, su kashe, su kuma hallaka kowace ƙungiyar mayaƙa, na kowace
ƙasa, ko lardi, da wataƙila za su kai musu, da matansu, da yaransu hari; su kuma
washe mallakar abokan gābansu. 12 Ranar da aka shirya domin Yahudawa su yi
wannan a dukan lardunan Sarki Zerzes, ita ce ranar goma sha uku ga watan goma
sha biyu, wato, watan Adar. 13 Za a ba da kofi na rubutacciyar dokar a matsayin
ƙa'ida a kowane lardi, a kuma sanar wa mutanen kowace ƙasa, domin Yahudawa su
zauna da shiri a ranar, domin su ɗau fansa a kan maƙiyansu.
14 'Yan aikan, a kan dawakan fada, suka fita a guje, umarnin sarki yana iza su. Aka
kuma ba da dokar a mazaunin masarauta wadda take Shusha.
15 Mordekai kuwa ya fita a gaban sarki da rigunan sarauta, masu ruwan shuɗi, da
fari, da babban kambi na zinariya, da alkyabba ta lilin mai ruwan shunayya. Aka
yi sowa don murna a birnin Shusha. 16 Ga Yahudawa kuwa, lokaci ne na murna da

† **7:9** Da Ibraniyanci kamu hamsin (wajen mita 23).

farin ciki, da jin daɗi da bangirma.
17 A kowane lardi da kowace birni, ko'ina da
dokar sarki ta kai, aka yi farin ciki a cikin Yahudawa, cike da bukukkuwa. Yawan mutane da waɗansu ƙasashe suka zama Yahudawa, don tsoron Yahudawa ya kama su.

# 9

*Nasarar Yahudawa*

1 A rana ta goma sha uku na watan goma sha biyu, wato, watan Adar ne za a aiwatar da dokar da sarki ya umarta. A wannan rana, abokan gāban Yahudawa suka sa zuciya za su sha ƙarfinsu, amma yanzu Zerzes ya canja, Yahudawa kuma suka yi galiba a bisa waɗanda suka ƙi jininsu.
2 Yahudawa suka tattaru a cikin biranensu a dukan lardunan Sarki Zerzes don su kai wa waɗanda suka nemi a hallaka su hari. Babu wanda ya tasar musu domin mutanen dukan sauran al'ummai sun jin tsoronsu.
3 Dukan sarakuna larduna, da hakimai, da gwamnoni da kuma ma'aikatan sarki suka taimaki Yahudawa, domin tsoron Mordekai ya kama su.
4 Mordekai babban mutum ne a fada, sunansa ya kai ko'ina a lardunan, ikonsa ya yi ta ƙasaita gaba-gaba.
5 Yahudawa suka karkashe dukan abokan gābansu da takobi, suka karkashe waɗanda suka ƙi jininsu, suka kuma hallaka su yadda suka ga dama.
6 A mazaunin masarautar a Shusha, Yahudawa suka karkashe, suka kuma hallaka mutum ɗari biyar.
7 Suka kuma kashe Farshandata, da Dalfon, da Asfata,
8 da Forata, da Adaliya, da Aridata,
9 da Farmashta, da Arisai, da Aridai da kuma Baizata,
10 'ya'ya maza goma na Haman ɗan Hammedata, abokin gāban Yahudawa. Amma ba su taɓa dukiyarsu ba.
11 A wannan rana, aka ba wa sarki rahoton yawan mutanen da aka kashe a mazaunin masarauta, a Shusha.
12 Sarki ya ce wa Sarauniya Esta, "Yahudawa sun karkashe, suka kuma hallaka mutum ɗari biyar, da kuma 'ya'ya maza goma na Haman a mazaunin masarauta a Shusha. Me suka yi a sauran lardunan sarki? Yanzu kuma mene ne roƙonki? Za a ba ki. Mece ce bukatarki? Za a biya miki."
13 Esta ta ce, "In sarki ya yarda, yă ba wa Yahudawa da suke Shusha izini su aikata dokan nan gobe kuma, bari kuma a rataye 'ya'ya maza goma na Haman a kan gumagumai."
14 Sai sarki ya ba da umarni a yi haka ɗin. Aka ba da doka a Shusha, aka kuma rataye 'ya'ya maza goma na Haman.
15 Yahudawan da suke Shusha suka taru a ran goma sha huɗu na watan Adar suka kuma karkashe mutum ɗari uku a Shusha, amma ba su taɓa dukiyarsu ba.
16 Ana cikin haka, sai saura Yahudawa waɗanda suke lardunan sarki su ma suka taru domin su kāre kansu su kuma sami hutu daga abokan gābansu. Suka karkashe mutum dubu saba'in da biyar amma ba su taɓa dukiyarsu ba.
17 Wannan ya faru a ran goma sha uku na watan Adar. A rana ta goma sha huɗu kuwa suka huta, suka kuma mai da ita ranar biki da kuma ta farin ciki.

*An kafa bikin Furim*

18 Amma Yahudawan da suke a Shusha suka taru a rana ta goma sha uku da ta sha huɗu, sa'an nan a rana ta goma sha biyar suka huta, suka kuma mai da ita ranar biki da ta farin ciki.
19 Shi ya sa Yahudawan ƙauyuka, waɗanda suke zama a karkara, suke kiyaye rana ta goma sha huɗu ta watan Adar a matsayin ranar farin ciki da ta biki, ranar ba da kyautai ga juna.
20 Sai Mordekai ya rubuta waɗannan abubuwa, ya kuma aika wasiƙu ga dukan Yahudawa ko'ina a lardunan Sarki Zerzes, na kusa da na nesa.
21 Ya sa su yi bikin kowace shekara a ranaku goma sha huɗu da goma sha biyar na watan Adar
22 a matsayin lokacin da Yahudawa suka sami huta daga abokan gābansu, da kuma a

matsayin watan da aka mai da baƙin cikinsu ya zama farin ciki, makokinsu kuma ya
zama ranar biki. Ya rubuta musu su kiyaye ranakun a matsayin ranakun biki da na
farin ciki. Su kuma ba da kyautai na abinci ga juna, da kuma kyautai ga matalauta.
23 Ta haka, Yahudawa suka yarda su ci gaba da bikin da suka fara, suna aikata abin
da Mordekai ya rubuta musu. 24 Haman ɗan Hammedata, mutumin Agag, abokin
gāban dukan Yahudawa, ya ƙulla maƙarƙashiya game da Yahudawa, domin a hallaka
su, ya kuma jefa *fur* (wato, ƙuri'a) don yă hallaka su. 25 Amma sa'ad da sarki ya
sami labarin maƙarƙashiyar,* sai ya ba da umarnai a rubuce cewa mugun shirin
da Haman ya ƙulla a kan Yahudawa yă komo kansa, kuma cewa a rataye shi da
'ya'yansa maza a kan gumagumai. 26 (Saboda haka, aka kira ranakun nan Furim,
daga kalma *fur*). Saboda dukan abin da aka rubuta cikin wannan wasiƙa da kuma
abin da suka gani, da abin da ya same su. 27 Yahudawa suka ɗauki nawayar kafa
al'adar cewa su, da zuriyarsu, da dukan waɗanda suka haɗa hannun da su, za su
kiyaye waɗannan kwanaki biyu, kowace shekara yadda aka tsara, a kuma lokacin
da aka keɓe dominsu. 28 Za a tuna, a kuma kiyaye waɗannan kwanaki a kowane
zamani, cikin kowane iyali, da kuma cikin kowane lardi, da kowace birni. Kuma
kada Yahudawa su fasa yin bikin waɗannan kwanakin Furim, ko su bar jikokinsu su
manta da kiyaye waɗannan ranaku biyu.
29 Saboda haka Sarauniya Esta, 'yar Abihayil, tare da Mordekai mutumin Yahuda,
suka rubuta da cikakken iko, suka tabbatar da wannan wasiƙa ta biyu game da Furim.
30 Mordekai kuwa ya aika da wasiƙu zuwa ga dukan Yahudawa cikin larduna 127
na masarautar Zerzes. Saƙon fatan alheri da na tabbaci, 31 don a kafa waɗannan
ranakun Furim a keɓaɓɓen lokacinsu, kamar yadda Mordekai mutumin Yahuda da
Sarauniya Esta suka dokace su. Yadda kuma suka kafa wa kansu da zuriyarsu, game
da lokutansu na azumi da makoki. 32 Dokar Esta ta tabbatar da waɗannan umarnai
game da Furim, aka kuma rubuta ta cikin tarihi.

# 10

*Girman Mordekai*
1 Sarki Zerzes ya sa a biya haraji a ko'ina a cikin daular, har zuwa ƙasashe masu
nesa na bakin teku. 2 Dukan ayyukan Sarki Zerzes masu iko da masu girma tare
da cikakken rahoton girmama Mordekai wanda sarki ya yi masa, ba a rubuce suke
a cikin littafin tarihin sarakunan Mediya da na Farisa ba? 3 Mordekai mutumin
Yahuda, shi ne na biyu a matsayi bayan Sarki Zerzes, mai farin ciki kuma a cikin
Yahudawa, aka kuma ɗauke shi da martaba cikin 'yan'uwansa Yahudawa. Gama ya
yi aiki don kyautatawar mutanensa, ya kuma yi magana don a kyautata rayuwar
dukan Yahudawa.

* **9:25** Ko kuwa sa'ad da Esta ta zo gaban sarki

# Ayuba

*Gabatarwa*

1 A ƙasar Uz akwai wani mutum mai suna Ayuba. Mutum ne marar laifi kuma mai
adalci; yana tsoron Allah, ba ruwansa da mugunta. 2 Yana da ʼyaʼya maza bakwai da
ʼyan mata uku, 3 yana da tumaki dubu bakwai, raƙuma dubu uku, shanu ɗari biyar,
da jakuna ɗari biyar, yana kuma da masu yi masa aiki da yawa. A ƙasar Gabas ba
wani kamar sa.
4 ʼYaʼyansa maza sukan yi biki a gidajensu, wannan yă yi yă ba wancan, sai su kira
ʼyanʼuwansu mata ukun su ci, su sha tare. 5 Bayan lokacin bikin ya wuce, sai Ayuba
yă aika su zo don yă tsarkake su. Tun da sassafe zai miƙa hadaya ta ƙonawa domin
kowannensu, don yana tunani cewa, "Mai yiwuwa ʼyaʼyana sun yi wa Allah zunubi,
ko sun laʼanta shi a cikin zuciyarsu." Haka Ayuba ya saba yi.

*Gwajin Ayuba na farko*

6 Wata rana malaʼiku[*] suka kawo kansu gaban Ubangiji, Shaiɗan[†] shi ma ya zo tare
da su. 7 Ubangiji ya ce wa Shaiɗan, "Daga ina ka fito?"
Shaiɗan ya amsa wa Ubangiji ya ce, "Daga yawo a duniya ina kai da kawowa a
cikinta."
8 Sai Ubangiji ya ce wa Shaiɗan, "Ko ka ga bawana Ayuba? A cikin duniya babu
wani kamar sa; shi marar laifi ne, adali kuma, mutum ne mai tsoron Allah, ba
ruwansa da mugunta."
9 Sai Shaiɗan ya amsa ya ce, "Haka kawai Ayuba yake tsoron Allah? 10 Ba ka kāre
shi da iyalinsa gaba ɗaya da duk mallakarsa ba? Ka Albarkaci ayyukan hannunsa
yadda dabbobinsa duk sun cika koʼina. 11 Ka ɗan miƙa hannunka ka raba shi da duk
abin da yake da shi, ba shakka zai laʼanta ka kana ji, kana gani."
12 Ubangiji ya ce wa Shaiɗan, "To, shi ke nan, duk abin da yake da shi yana
hannunka, amma kada ka taɓa shi, shi kansa."
Sai Shaiɗan ya bar Ubangiji.
13 Wata rana lokacin da ʼyaʼyan Ayuba suke cikin biki a gidan babban ɗansa, 14 sai
ɗan aika ya zo wurin Ayuba ya ce masa, "Shanu suna huɗa, jakuna kuma suna kiwo
nan kusa, 15 sai Sabenawa suka auka musu suka kwashe su suka tafi, suka karkashe
masu yi maka aiki duka, ni kaɗai na tsira na zo in gaya maka!"
16 Yana cikin magana sai ga wani ɗan aika ya zo ya ce, "Wutar Allah ta sauko daga
sama ta ƙona dukan tumaki da masu lura da su, wato, bayinka, ni kaɗai na tsira na
zo in gaya maka!"
17 Yana cikin magana sai ga wani ɗan aika ya zo ya ce, "Kungiyoyin mahara uku
na Kaldiyawa sun auka wa raƙumanka sun kwashe su duka, suka kuma karkashe
masu yi maka aiki, ni kaɗai ne na tsira na zo in gaya maka!"
18 Yana cikin magana, sai ga wani ɗan aika ya zo ya ce, "ʼYaʼyanka maza da mata
suna biki, suna ci suna sha a gidan babban ɗanka, 19 sai wata iska mai ƙarfi daga
hamada ta auka ta rushe gidan, gidan kuwa ya fāɗi a kan ʼyaʼyanka ya kashe su, ni
kaɗai na tsira na zo in gaya maka!"
20 Da jin haka sai Ayuba ya tashi ya yayyaga tufafin jikinsa, ya aske kansa. Ya fāɗi
a ƙasa ya yi sujada 21 ya ce,
"Tsirara na fito daga cikin mahaifiyata,
tsirara kuma zan koma.

[*] **1:6** Da Ibraniyanci ʼyaʼyan Allah maza [†] **1:6** Shaiɗan yana nufin mai zargi.

UBANGIJI ya bayar, UBANGIJI kuma ya karɓa;
yabo ya tabbata ga UBANGIJI."
22 Cikin wannan duka Ayuba bai yi wa Allah zunubi ta wurin ba shi laifi ba.

# 2

### *Gwajin Ayuba na biyu*

1 Wata rana kuma mala'iku suka sāke kawo kansu gaban UBANGIJI, sai Shaiɗan shi
ma ya zo tare da su yă nuna kansa a gabansa. 2 Sai UBANGIJI ya ce wa Shaiɗan, "Daga
ina ka fito?"
Shaiɗan ya amsa wa UBANGIJI ya ce, "Daga yawo a duniya ina kai da kawowa a
cikinta."
3 Sai UBANGIJI ya ce wa Shaiɗan, "Ko ka ga bawana Ayuba? A cikin duniya babu
wani kamar sa; shi marar laifi ne, adali kuma, mutum ne mai tsoron Allah ba ruwansa
da mugunta. Kuma har yanzu bai fasa zama mai aminci ba duk da wahalar da ka sa
na bari ka ba shi ba tare da wani dalili ba."
4 Shaiɗan ya amsa ya ce, "Fata don fata! Mutum zai iya rabuwa da duk abin da
yake da shi domin ransa. 5 Ka ɗan taɓa lafiyar jikinsa ka gani ba shakka zai la'anta
ka kana ji kana gani."
6 UBANGIJI ya ce wa Shaiɗan, "To, shi ke nan, duk abin da yake da shi yana
hannunka, amma kada ka taɓa shi, shi kansa."
7 Sai Shaiɗan ya bar UBANGIJI, ya je ya sa wa Ayuba ƙuraje masu zafi a jikinsa daga
tafin ƙafafunsa har zuwa kansa. 8 Sai Ayuba ya ɗauki kaskon tukunya yana ta sosa
ƙurajen da shi, yayinda yake zaune cikin toka.
9 Matarsa ta ce masa, "Har yanzu kana nan da amincinka? Ka la'anta Allah ka
mutu!"
10 Ya amsa ya ce, "Kina magana kamar wawiya. Alheri kaɗai za mu dinga samu
daga Allah ban da wahala?"
A cikin wannan duka Ayuba bai yi zunubi ba cikin maganarsa.

### *Abokan Ayuba uku*

11 Lokacin da abokan Ayuba su uku wato, Elifaz mutumin Teman, Bildad mutumin
Shuwa, da Zofar mutumin Na'ama suka ji wahalar da ta auka wa Ayuba, sai suka
shirya suka bar gidajensu suka je don su ta'azantar da shi. 12 Sa'ad da suka gan shi
daga nesa, da ƙyar suka gane shi; sai suka fara kuka da ƙarfi, suka yayyaga tufafinsu
suka zuba toka a kawunansu, 13 sai suka zauna da shi a ƙasa har kwana bakwai. Ba
wanda ya ce masa kome, don sun ga tsananin wahalar da yake ciki.

# 3

### *Ayuba ya yi magana*

1 Bayan wannan Ayuba ya buɗe baki ya la'anta ranar da aka haife shi. 2 Ayuba ya
ce,
3 "A hallaka ranar da aka haife ni,
da kuma daren da aka ce, 'An haifi jariri namiji!'
4 Bari ranan nan ta zama duhu;
kada Allah yă kula da ita;
kada rana tă yi haske a wannan rana.
5 Bari duhu da inuwa mai duhu ta sāke rufe ta;
gizagizai kuma su rufe ta;
duhu kuma ya rufe haskenta.
6 Bari duhu mai yawa yă rufe daren nan;

kada a haɗa ta cikin kwanakin shekara,
ko kuma cikin kwanakin watanni.
7 Bari daren yă zama marar amfani;
kada a ji wata sowa ta farin ciki.
8 Bari waɗanda suke la'anta ranaku su la'anta wannan rana
su waɗanda suke umartar dodon ruwa.
9 Bari taurarinta na safe su zama duhu;
bari ranar tă yi ta jiran ganin haske
amma kada tă gani,
10 gama ba tă hana uwata ɗaukar cikina,
don ta hana ni shan wahalan nan ba.

11 "Me ya sa ban mutu ba da za a haife ni,
ko kuma in mutu sa'ad da ana haihuwata ba?
12 Me ya sa aka haife ni,
aka tanada nono na sha na rayu?
13 Da yanzu ina kwance cikin salama;
da ina barcina cikin salama
14 tare da sarakuna da mashawarta a cikin ƙasa,
waɗanda suka gina wa kansu wuraren da yanzu duk sun rushe,
15 da shugabanni waɗanda suke da zinariya,
waɗanda suka cika gidajensu da azurfa.
16 Ko kuma don me ba a ɓoye ni a cikin ƙasa kamar jaririn da aka haifa ba rai ba,
kamar jaririn da bai taɓa ganin hasken rana ba.
17 A wurin mugaye za su daina yin mugunta,
gajiyayyu kuma za su huta.
18 Waɗanda aka daure za su sami jin daɗin;
an sake su ba za su sāke jin ana tsawata masu ba.
19 Manyan da ƙanana suna a can,
bawa kuma ya sami 'yanci daga wurin maigidansa.

20 "Don me ake ba da haske ga waɗanda suke cikin ƙunci,
rai kuma ga masu ɗacin rai
21 ga waɗanda suke neman mutuwa amma ba su samu ba,
waɗanda suke nemanta kamar wani abu mai daraja a ɓoye,
22 waɗanda suke farin ciki
sa'ad da suka kai kabari?
23 Don me aka ba mutum rai,
mutumin da bai san wani abu game da kansa ba,
mutumin da Allah ya kange shi.
24 Baƙin ciki ya ishe ni maimakon abinci;
ina ta yin nishi ba fasawa;
25 Abin da nake tsoro ya faru da ni;
abin da ba na so ya same ni.
26 Ba ni da salama, ba natsuwa;
ba ni da hutu, sai wahala kawai."

# 4

*Elifaz*

1 Sai Elifaz mutumin Teman ya amsa,
2 "In wani ya yi maka magana, za ka ji haushi?
Amma wa zai iya yin shiru?

3 Ka tuna yadda ka yi wa mutane da yawa magana,
yadda ka ƙarfafa hannuwa marasa ƙarfi.
4 Maganarka ta ƙarfafa waɗanda suka yi tuntuɓe;
ka ƙarfafa gwiwoyin da suka rasa ƙarfinsu.
5 Amma yanzu wahala ta zo maka, sai ka karaya;
wahala ta sa ka rikice.
6 Ashe bai kamata ka dogara ga Allahnka ba,
amincinka kuma yă zama begenka?

7 “Ka duba ka gani yanzu. Wane marar laifi ne ya taɓa hallaka?
Ko an taɓa hallaka masu adalci?
8 Na kula cewa waɗanda suke huɗa gonar mugunta,
da waɗanda suke shuka mugunta, su ne suke girbe mugunta.
9 A sa’a ɗaya Allah yake hallaka su,
cikin fushinsa yakan hallaka su.
10 Zakoki suna ruri suna gurnani;
duk da haka an karya haƙoran manyan zakoki.
11 Zakoki suna mutuwa domin ba dabbar da za su kashe su ci,
’ya’yan zakanya kuma sun watse.

12 “Asirce aka gaya mini maganan nan,
da ƙyar kunnuwana suka iya ji.
13 Cikin mafarki da tsakar dare,
lokacin kowa yana zurfin barci, na sami saƙon nan.
14 Tsoro da fargaba suka kama ni
har duk ƙasusuwan jikina suka yi ta rawa.
15 Wani iska ya taɓa mini fuska,
sai tsigar jikina ta tashi.
16 Ya tsaya cik,
amma ban iya sani ko mene ne ba.
Wani abu ya tsaya a gabana,
na kuma ji murya.
17 ‘Ko zai yiwu mutum yă fi Allah adalci,
ko kuma mutum yă fi wanda ya halicce shi tsarki?
18 In Allah bai yarda da bayinsa ba,
in ya sami mala’ikunsa da laifi,
19 to, su wane ne mutane masu zama a gidan da aka yi da laka,
waɗanda da ƙura aka yi harsashensu,
waɗanda za a iya murƙushe su kamar asu!
20 Tsakanin safe da yamma mai yiwuwa ne ragargaza su;
farat ɗaya, su mutu har abada.
21 Ba a tuge igiyar tentinsu,
don su mutu ba tare da hikima ba?’

# 5

1 “Ka yi kira in kana so, amma wa zai amsa maka?
Wurin waɗanne tsarkaka za ka juya?
2 Fushi yana kashe wawa,
ƙyashi kuma yana kashe marar azanci.
3 Ni ma na ga wawa yana cin gaba,

amma nan da nan gidansa ya zama la’ananne.
4 ’Ya’yansa suna cikin hatsari,
ba wanda zai tsaya musu a gaban alƙali,
5 mayunwata sun kwashe girbinsa,
har abubuwan da suke cikin ƙaya,
masu jin ƙishirwa kuma suna zuba ido ga dukiyarsa.
6 Gama ba daga cikin ƙasa wahala take fitowa ba,
ko kuma bala’i daga ƙasa.
7 Duk da haka an haifi mutum don wahala ne,
kamar yadda ba shakka tartsatsin wuta yake tashi.

8 “Amma da a ce ni ne, da zan roƙi Allah;
zan gaya masa damuwata.
9 Yana yin abubuwan al’ajabi waɗanda ba a ganewa,
mu’ujizai waɗanda ba a ƙirgawa.
10 Yana zuba ruwan sama a ƙasa;
yana zuba ruwa a gonaki.
11 Yana ɗaukaka masu sauƙinkai,
yana kāre waɗanda suke makoki.
12 Yana dagula shirye-shiryen masu wayo
don kada su yi nasara cikin abubuwan da suke shirin yi.
13 Yana kama masu wayo cikin wayonsu,
yana kawar da shirye-shiryensu ba za su yi nasara ba.
14 Da rana sukan yi karo da duhu;
da rana ma suna lallube kamar a duhun dare suke.
15 Yana ceton matalauta daga takobin da za tă kashe su da shi;
yana cetonsu daga hannun waɗanda suka fi su ƙarfi.
16 Saboda haka matalauta suna da bege,
rashin gaskiya kuma ta yi shiru.

17 “Mai albarka ne wanda Allah yake yi masa gyara in mutumin ya yi kuskure;
saboda haka kada ka guje wa horon Maɗaukaki.
18 Ko da yake yana sa ciwo, shi ne kuma yake warkar da ciwon;
ciwon da ya ji maka, shi da kansa zai warkar da shi.
19 Zai cece ka daga bala’o’i guda shida;
har bakwai ma ba abin da zai same ka.
20 Lokacin yunwa yana tsare ka daga mutuwa,
a cikin yaƙi kuma yana kāre ka daga sarar takobi.
21 Zai kāre ka daga ɓata suna,
kuma ba ka bukata ka ji tsoro in hallaka ta zo.
22 Za ka yi wa hallaka da yunwa dariya;
kuma ba ka bukata ka ji tsoron manyan namun jeji.
23 Gama za ka zauna lafiya da duwatsu a gonaki,
kuma manyan namun jeji za su yi zaman salama da kai.
24 Za ka zauna lafiya a cikin tenti naka,
za ka ƙirga kayanka za ka samu kome na nan.
25 Za ka san cewa ’ya’yanka za su zama da yawa,
zuriyarka kuma kamar ciyawa a ƙasa.
26 Za ka yi kyakkyawan tsufa kafin ka mutu,
kamar yadda ake tara dammuna a lokacin girbi.

27 “Mun yi nazarin wannan, kuma gaskiya ne.
Saboda haka ka ji, ka kuma yi amfani da shi.”

# 6

*Ayuba*

1 Sa’an nan Ayuba ya amsa,
2 “Da kawai za a iya auna wahalata
a kuma sa ɓacin raina a ma’auni!
3 Ba shakka da sun fi yashin teku nauyi,
shi ya sa nake magana haka.
4 Kibiyoyin Maɗaukaki suna a kaina,
ruhuna yana shan dafinsa;
fushin Allah ya sauka a kaina.
5 Jaki yakan yi kuka sa’ad da ya sami ciyawar ci,
ko saniya takan yi kuka in ta sami abincinta?
6 Akan cin abinci marar ɗanɗano ba tare da an sa gishiri ba,
ko akwai wani ƙanshin daɗi a cikin farin ruwan ƙwai?
7 Na ƙi in taɓa shi;
irin wannan abinci zai sa ni rashin lafiya.

8 “Kash, da ma Allah zai ba ni abin da nake fatar samu,
da ma Allah zai biya mini bukatata,
9 wato, Allah yă kashe ni,
yă miƙa hannunsa yă yanke raina!
10 Da sai in ji daɗi
duk zafin da nake sha
ban hana maganar Mai Tsarkin nan cika ba.

11 “Wane ƙarfi nake da shi, har da zan ci gaba da sa zuciya?
Wane sa zuciya ne zai sa in yi haƙuri?
12 Da ƙarfin dutse aka yi ni ne?
Ko jikina tagulla ne?
13 Ina da wani ikon da zan iya taimakon kai na ne,
yanzu da aka kore nasara daga gare ni?

14 “Duk wanda ya ƙi yă yi alheri ga aboki
ya rabu ta tsoron Maɗaukaki.
15 Amma ’yan’uwana sun nuna ba zan iya dogara gare su ba,
kamar rafin da yakan bushe da rani,
16 kamar rafin da yakan cika a lokacin ƙanƙara,
yă kuma kumbura kamar ƙanƙarar da ta narke,
17 amma da rani sai yă bushe,
lokacin zafi ba a samun ruwa yana gudu a wurin.
18 Ayari sukan bar hanyarsu;
sukan yi ta neman wurin da za su sami ruwa, su kāsa samu har su mutu.
19 Ayarin Tema sun nemi ruwa,
matafiya ’yan kasuwa Sheba sun nema cike da begen samu.
20 Ransu ya ɓace, domin sun sa zuciya sosai;
sa’ad da suka kai wurin kuwa ba su sami abin da suka sa zuciyar samu ba.
21 Yanzu kuma kun nuna mini ba ku iya taimako;

kun ga abin bantsoro kuka tsorata.
22 Ko na taɓa cewa, ‘Ku ba da wani abu a madadina,
ko na roƙe ku, ku ba da wani abu domina daga cikin dukiyarku,
23 ko kuma kun taɓa kuɓutar da ni daga hannun maƙiyina,
ko kun taɓa ƙwato ni daga hannun marasa kirki’?

24 “Ku koya mini, zan yi shiru;
ku nuna mini inda ban yi daidai ba.
25 Faɗar gaskiya tana da zafi!
Amma ina amfanin gardamar da kuke yi?
26 Ko kuna so ku gyara abin da na faɗi ne,
ku mai da magana wanda yake cikin wahala ta zama ta wofi?
27 Kukan yi ƙuri’a a kan marayu
ku kuma sayar da abokinku.

28 “Amma yanzu ku dube ni da kyau,
zan yi muku ƙarya ne?
29 Ku bi a hankali, kada ku ɗora mini laifi;
ku sāke dubawa, gama ba ni da laifi.
30 Ko akwai wata mugunta a bakina?
Bakina ba zai iya rarrabewa tsakanin gaskiya da ƙarya ba?

# 7

1 “Mutum bai sha wahalar aiki ba a duniya?
Rayuwarsa ba kamar ta wanda aka yi hayarsa ba ne?
2 Kamar yadda bawa yakan jira yamma ta yi,
ko kuma kamar yadda wanda aka yi hayarsa yakan jira a biya shi kuɗin aikin da ya yi.
3 Saboda haka rabona shi ne watanni na zama banza,
kowane dare kuwa sai ɓacin rai nake samu.
4 Lokacin da na kwanta ina tunani, ‘Har sai yaushe zan tashi?’
Gari ya ƙi wayewa, ina ta jujjuyawa har safe.
5 Jikina duk tsutsotsi da ƙuraje sun rufe shi,
fatar jikina ta ruɓe tana fitar da ruwan miki.

6 “Kwanakina suna wucewa da sauri, fiye da yadda ƙoshiyar masaƙa take wucewa da sauri,
za su kawo ga ƙarshe ba bege.
7 Ka tuna, ya Allah, raina numfashi ne kawai;
idanuna ba za su taɓa sāke ganin farin ciki ba.
8 Idanun da suke ganina yanzu ba za su sāke ganina ba;
za ku neme ni amma ba za ku same ni ba.
9 Kamar yadda girgije yakan ɓace yă tafi,
haka mutum yake shige zuwa kabari ba kuwa zai dawo ba.
10 Ba zai taɓa zuwa gidansa ba;
ba za a sāke san da shi ba.

11 “Saboda haka ba zan yi shiru ba;
zan yi magana cikin ɓacin raina,
zan nuna ɓacin raina cikin ruhu, cikin ƙuncin raina.

12 Ni teku ne, ko kuwa dodon ruwa,
don me kake tsaro na?
13 Lokacin da nake zato zan sami salama
in na kwanta a gadona don in huta,
14 duk da haka kana ba ni tsoro da mafarke-mafarke,
kana tsorata ni da wahayi.
15 Na gwammace a shaƙe ni in mutu
maimakon in kasance cikin wannan jiki.
16 Ba na so in zauna da rai; ba zan rayu ba har abada.
Ku rabu da ni; rayuwata ba ta da amfani.

17 “Mene ne mutum har da ka kula da shi haka,
har ka mai da hankali a kansa,
18 har kake duba shi kowace safiya,
kake kuma gwada shi koyaushe?
19 Ba za ka ɗan daina kallo na ba
ko ka rabu da ni na ɗan lokaci?
20 In na yi zunubi, me na yi maka,
kai mai lura da mutane?
Don me ka sa ni a gaba?
Na zame maka kaya mai nauyi ne?
21 Me ya sa ba za ka gafarta mini laifofina ba?
Gama na kusa kwantawa cikin ƙasa;
za ka neme ni,
amma ba za ka same ni ba.”

# 8

*Bildad*

1 Sai Bildad mutumin Shuwa ya amsa,
2 “Har yaushe za ka gama faɗa waɗannan abubuwa?
Maganganunka ba su da amfani.
3 Allah ba mai shari’ar gaskiya ba ne?
Ko Maɗaukaki yakan yi abin da ba daidai ba?
4 Lokacin da ’ya’yansa suka yi masa zunubi,
yakan bar su su sha wahalar da zunubi yake kawowa.
5 Amma in za ka dubi Allah
ka roƙi Maɗaukaki,
6 in kai mai tsarki ne, kuma mai adalci,
ko yanzu ma zai taimake ka,
yă mayar maka iyalinka da farin cikinka.
7 Ko da yake za ka fara da kaɗan,
duk da haka za ka gama da samu mai yawa.

8 “Tambayi na gaba da kai
ka ji abin da iyayenka suka koya
9 gama jiya kaɗai aka haife mu ba mu san kome ba,
kuma kwanakinmu a duniya masu wucewa ne.
10 Ba za su bishe ka su kuma gaya maka abin da za ka yi ba?
Ba za su yi magana daga cikin hikimar da suke da ita ba?
11 Ko kyauro zai iya yi girma a wurin da ba ruwa?
Ko za tă taɓa iya yin girma ba tare da ruwa ba?
12 Yayinda take girma ba a yanka ta,

takan mutu da sauri fiye da ciyawa.
13 Abin da yake faruwa ke nan da duk wanda yake mantawa da Allah;
wa'danda ba su da Allah, ba su da bege.
14 Abin da yake dogara a kai ba shi da ƙarfi;
abin da yake dogara a kai yanar gizo ce.
15 Ya jingina ga yanar gizo, amma ba ta tare shi,
sun kama ta, amma ba za tă taimake su tsayawa ba.
16 Yana kama da shukar da aka ba ta ruwa sosai lokacin da akwai rana sosai,
tana yaɗuwa da kyau;
17 shukar tana bin yaɗuwa, jijiyoyinta suna nannaɗe duwatsu,
suna neman wurin da za su kama sosai a cikin duwatsu.
18 Amma lokacin da aka tuge shukar daga wurin da take,
wurin ba zai san da ita kuma ba, wurin zai ce, 'Ban taɓa ganin ki ba.'
19 Ba shakka shukar ta mutu ke nan,
kuma waɗansu za su tsiro a wurin.

20 "Ba shakka, Allah ba ya ƙin marar laifi,
ko kuma yă ƙarfafa masu aikata mugunta.
21 Sai dai yă cika bakinka da dariya,
yă sa ka yi sowa ta murna.
22 Maƙiyanka za su sha kunya,
za a kawar da tentin mugaye."

# 9

*Ayuba*

1 Sai Ayuba ya amsa,
2 "Lalle, na san wannan gaskiya ne.
Amma ta yaya mutum zai iya zama mai adalci a gaban Allah?
3 Ko da mutum yana so yă yi gardama da shi,
ba zai taɓa amsa masa ba ko da sau ɗaya cikin dubu.
4 Hikimarsa tana da zurfi, ikonsa yana da yawa.
Wane ne ya taɓa yin faɗa da shi har ya yi nasara?
5 Yana matsar da manyan duwatsu kafin su sani
kuma yana juya su cikin fushinsa.
6 Yana girgiza ƙasa,
yana girgiza harsashenta.
7 Yana magana da rana sai ta ƙi yin haske;
yana hana taurari yin haske.
8 Shi kaɗai ya shimfiɗa sammai
ya kuma yi tafiya a kan raƙuman ruwan teku.
9 Shi ne ya halicci Mafarauci da Kare da Zomo, da Kaza,
da 'Ya'yanta da tarin taurari a sama, da taurarin kudu.
10 Yana yin abubuwan banmamaki waɗanda ba a iya ganewa,
mu'ujizai waɗanda ba a iya ƙirgawa.
11 Ba na iya ganinsa lokacin da ya wuce ni;
ba na sani ya wuce lokacin da ya wuce.
12 Wane ne ya isa yă hana shi in ya ƙwace abu?
Wa zai ce masa, 'Me kake yi?'
13 Allah ba ya danne fushinsa;
ko dodannin ruwan da ake kira ayarin Rahab ya tattake su.

14 “Ta yaya zan iya yin faɗa da shi?
Ina zan iya samun kalmomin da zan yi gardama da shi?
15 Ko da yake ba ni da laifi, ba zan iya amsa masa ba;
sai dai roƙon jinƙai zan iya yi ga mahukuncina.
16 Ko da na yi kira gare shi ya amsa mini,
ban yarda cewa zai saurare ni ba.
17 Zai sa hadari yă danne ni
yă ƙara mini ciwona ba dalili.
18 Ba zai bari in yi numfashi ba,
sai dai yă ƙara mini azaba.
19 In maganar ƙarfi ne, shi babban mai ƙarfi ne!
In kuma maganar shari’a ne, wa zai kai kararsa?
20 Ko da ni marar ƙarfi ne, bakina ya isa yă sa in zama mai laifi;
in ba ni da laifi, zai sa in yi laifi.

21 “Ko da yake ba ni da laifi,
ban damu da kaina ba;
na rena raina.
22 Ba bambanci; shi ya sa na ce,
‘Yana hallaka marasa laifi da kuma mugaye.’
23 Lokacin da bala’i ya kawo ga mutuwa,
yakan yi dariyar baƙin cikin marasa laifi.
24 Lokacin da ƙasa ta faɗa a hannun mugaye,
yakan rufe idanun masu shari’a.
In ba shi ba wa zai yi wannan?

25 “Kwanakina sun fi mai gudu wucewa da sauri;
suna firiya babu wani abin jin daɗi a cikinsu.
26 Suna wucewa kamar jirgin ruwan da aka yi da kyauro,
kamar jahurma da ta kai wa namanta cafka.
27 ‘In na ce zan manta da abin da yake damu na,
zan yi murmushi in daina nuna ɓacin rai,’
28 duk da haka ina tsoron duk wahalata,
domin na san ba za ka ɗauke ni marar laifi ba.
29 Tun da an riga an ɗauke ni mai laifi,
duk ƙoƙarina a banza yake.
30 Ko da na wanke jikina duka da sabulu,
na wanke hannuwana kuma da soda,
31 duk da haka za ka jefa ni cikin ƙazamin wuri,
yadda ko rigunan jikina ma za su ƙi ni.

32 “Shi ba mutum ba ne kamar ni wanda zan iya amsa masa,
har da za mu yi faɗa da juna a wurin shari’a.
33 In da akwai wanda zai iya shiga tsakaninmu,
ya ɗora hannunsa a kanmu tare,
34 wani wanda zai sa Allah yă daina duka na,
don yă daina ba ni tsoro.
35 Sa’an nan ne zan iya yin magana ba tare da jin tsoronsa ba,
amma a yadda nake a yanzu ba zan iya ba.

# 10

1 “Na gaji da rayuwa;
saboda haka bari in faɗi zuciyata gabagadi
yadda raina yake jin ba daɗi.
2 Zan ce wa Allah, kada ka hukunta ni,
amma ka gaya mini laifin da na yi maka.
3 Kana jin daɗin ba ni wahala,
don me ka yashe ni, abin da ka halitta da hannunka,
yayinda kake murmushi game da shirye-shiryen mugaye?
4 Idanunka irin na mutum ne?
Kana gani yadda mutum yake gani ne?
5 Kwanakinka kamar na mutane ne,
ko shekarunka kamar na mutane ne
6 da za ka neme ni da laifi
ka hukunta ni?
7 Ko da yake ka san ba ni da laifi,
kuma ba wanda zai iya cetona daga hannunka.

8 “Da hannuwanka ka ƙera ni, kai ka halicce ni.
Yanzu kuma kai za ka juya ka hallaka ni?
9 Ka tuna cewa ka mulmula ni kamar yumɓu.
Yanzu za ka mai da ni in zama ƙura kuma?
10 Ba kai ka zuba ni kamar madara ba,
na daskare kamar cuku.
11 Ka rufe ni da tsoka da fata,
ka harhaɗa ni da ƙasusuwa da jijiyoyi?
12 Ka ba ni rai ka kuma yi mini alheri,
kuma cikin tanadinka ka kula da ruhuna.

13 “Amma wannan shi ne abin da ka ɓoye a zuciyarka,
na kuma san abin da yake cikin zuciyarka ke nan.
14 In na yi zunubi kana kallo na
kuma ba za ka fasa ba ni horo ba don laifin da na yi.
15 Idan ina da laifi, kaitona!
Ko da ba ni da laifi, ba zan iya ɗaga fuskata ba,
gama kunya ta ishe ni
duk ɓacin rai ya ishe ni.
16 In na ɗaga kaina, za ka neme ni kamar zaki
ka sāke nuna al’ajabin ikonka a kaina.
17 Kana sāke kawo sababbin waɗanda za su ba da shaida a kaina
kana ƙara haushinka a kaina;
kana ƙara kawo mini hari.

18 “Me ya sa ka fito da ni daga cikin uwata?
Da ma na mutu kafin a haife ni.
19 Da ma ba a halicce ni ba,
da na mutu tun daga cikin cikin uwata na wuce zuwa kabari!
20 ’Yan kwanakina ba su kusa ƙarewa ba ne?
Ka rabu da ni don in ɗan samu sukuni na ɗan lokaci
21 kafin in koma inda na fito,
ƙasa mai duhu da inuwa sosai,
22 zuwa ƙasa mai duhun gaske,
da inuwa da hargitsi,

inda haske yake kamar duhu."

# 11

*Zofar*

1 Sa'an nan Zofar mutumin Na'ama ya amsa,
2 "Duk surutun nan ba za a amsa maka ba?
Ko mai surutun nan marar laifi ne?
3 Ko maganganun nan naka marasa amfani za su sa mutane su yi maka shiru?
Ba wanda zai kwaɓe ka lokacin da kake faɗar maganar da ba daidai ba?
4 Ka ce wa Allah, 'Abin da na gaskata ba laifi ba ne
kuma ni mai tsabta ne a gabanka.'
5 Da ma Allah zai yi magana,
yǎ buɗe baki yǎ faɗi wani abin da ka yi da ba daidai ba
6 yǎ kuma buɗe maka asirin hikima,
gama hikima ta gaskiya tana da gefe biyu.
Ka san wannan, Allah ya riga ya manta da waɗansu zunubanka.

7 "Ko za ka iya gane al'amuran Allah?
Ko za ka iya gane girman asirin Maɗaukaki?
8 Sun fi nisan sama tudu, me za ka iya yi?
Sun fi zurfin kabari zurfi, me za ka sani?
9 Tsayinsu ya fi tsawon duniya
da kuma fāɗin teku.

10 "In ya zo ya kulle ka a kurkuku
ya ce kai mai laifi ne, wa zai hana shi?
11 Ba shakka yana iya gane mutanen da suke marasa gaskiya;
kuma in ya ga abin da yake mugu, ba ya kula ne?
12 Amma daƙiƙin mutum ba ya taɓa zama mai hikima
kamar dai a ce ba a taɓa haihuwar ɗan aholaki horarre.

13 "Duk da haka in ka miƙa masa zuciyarka,
ka kuma miƙa hannuwanka gare shi,
14 in ka kawar da zunubin da yake hannunka,
ba ka bar zunubi ya kasance tare da kai ba
15 shi ne za ka iya ɗaga fuskarka ba tare da jin kunya ba;
za ka tsaya da ƙarfi kuma ba za ka ji tsoro ba.
16 Ba shakka za ka manta da wahalolinka,
za ka tuna da su kamar yadda ruwa yake wucewa.
17 Rayuwarka za tǎ fi hasken rana haske,
duhu kuma zai zama kamar safiya.
18 Za ka zauna lafiya, domin akwai bege;
za ka duba kewaye da kai ka huta cikin kwanciyar rai.
19 Za ka kwanta, ba wanda zai sa ka ji tsoro,
da yawa za su zo neman taimako a wurinka.
20 Amma idanun mugaye ba za su iya gani ba,
kuma ba za su iya tserewa ba;
begensu zai zama na mutuwa."

# 12

*Ayuba*

1 Sai Ayuba ya amsa,
2 “Ba shakka ku ne mutanen nan,
hikima za tă mutu tare da ku!
3 Amma ni ma ina da hankali kamar ku;
ba ku fi ni ba.
Wane ne bai san duk waɗannan abubuwan ba?

4 “Na zama abin dariya ga abokaina,
ko da yake na yi kira ga Allah ya kuwa amsa mini,
duk da haka suka yi mini riya ko da yake ni mai adalci ne kuma marar laifi!
5 Mutanen da ba su da damuwa suna jin daɗin ganin waɗanda
suke dab da fāɗuwa.
6 Amma wurin zaman ’yan fashi yana nan ba mai damunsu,
waɗanda kuma suke saɓa wa Allah suna zamansu lafiya,
har ma da masu ɗaukar allahnsu a hannuwansu.

7 “Amma ka tambayi dabbobi, za su kuma koya maka,
ko kuma tsuntsayen sararin sama kuma za su gaya maka.
8 Ko ka yi magana da duniya, za tă kuma koya maka,
ko kuma ka bar kifin teku su sanar da kai.
9 Wane ne cikin waɗannan bai san
cewa hannun Ubangiji ne ya yi wannan ba?
10 Ran kowace halitta yana a hannunsa,
haka kuma numfashin dukan ’yan adam.
11 Ko kunne ba ya gwada kalmomi
kamar yadda harshe yake ɗanɗana abinci?
12 Ko ba a wurin tsofaffi ake samun hikima ba?
Ba tsawon rai yana kawo ganewa ba?

13 “Allah ne mai iko da kuma hikima,
shawara da ganewa nasa ne.
14 Abin da ya rushe ba a iya ginawa ba;
in ya kulle mutum ba a iya buɗe shi a sake shi ba.
15 Idan ya hana ruwan sama, za a yi fări;
in kuma ya saki ruwa za a yi ambaliya.
16 Shi ne mai ƙarfi da kuma mai nasara;
mai ruɗi da wanda aka ruɗa, duk nasa ne.
17 Yakan sa mashawarta su zama marasa hikima
yă kuma sa wawaye su zama masu shari’a.
18 Yana cire sarƙar da sarakuna suka ɗaura
yă kuma ɗaura musu wata tsumma a kwankwaso.
19 Yakan ƙasƙantar da firistoci
yă kuma tumɓuke masu ikon da aka kafa tun da daɗewa.
20 Yana sa amintattun mashawarta su yi shiru
yakan kawar da hikimar dattawa.
21 Yakan sa masu iko su ji kunya
yă kuma ƙwace ƙarfin masu ƙarfi.
22 Yana buɗe abubuwan da suke cikin duhu
yă kuma kawo haske a wuraren da ba haske;
23 yana sa al’ummai su zama manya, sai kuma yă hallaka su;

yana sa al'ummai su ƙasaita, yă kuma watsar da su.
24 Yana hana shugabannin duniya ganewa;
Ya bar su su yi ta makuwa, su ruɗe, su ɓata.
25 Suna lallube cikin duhu ba haske;
yă sa su yi ta tangaɗi kamar bugaggu.

# 13

1 "Idanuna sun ga waɗannan duka,
kunnuwana sun ji sun kuma gane.
2 Abin da kuka sani, ni ma na sani;
ba ku fi ni ba.
3 Amma ina so in yi magana da Maɗaukaki,
in kai kukana wurin Allah kai tsaye.
4 Ku kuma kun ishe ni da ƙarairayi;
ku likitocin wofi ne, dukanku!
5 In da za ku yi shiru gaba ɗaya!
Zai zama muku hikima.
6 Ku ji gardamata yanzu;
ku ji roƙon da zai fito daga bakina.
7 Za ku iya yin muguwar magana a madadin Allah?
Ko za ku yi ƙarya a madadinsa?
8 Ko za ku nuna masa sonkai?
Ko za ku yi gardama a madadinsa?
9 In ya bincike ku zai tarar ba ku da laifi?
Ko za ku iya ruɗe shi yadda za ku ruɗi mutane?
10 Ba shakka zai kwaɓe ku
in kun nuna sonkai a ɓoye.
11 Ko ikonsa ba ya ba ku tsoro?
Tsoronsa ba zai auka muku ba?
12 Duk surutanku kamar toka suke;
kāriyarku na yimɓu ne.

13 "Ku yi shiru zan yi magana;
sa'an nan abin da zai same ni yă same ni.
14 Don me na sa kaina cikin hatsari
na yi kasada da raina?
15 Ko da zai kashe ni ne, begena a cikinsa zai kasance;
ba shakka zan kāre kaina a gabansa
16 lalle wannan zai kawo mini kuɓuta
gama ba wani marar tsoron Allah da zai iya zuwa wurinsa!
17 Ku saurara da kyau ku ji abin da zan faɗa;
bari kunnuwanku su ji abin da zan ce.
18 Yanzu da na shirya ƙarata,
na san za a ce ba ni da laifi.
19 Ko wani zai ce ga laifin da na yi?
In an same ni da laifi, zan yi shiru in mutu.

20 "Kai dai biya mini waɗannan bukatu biyu kawai ya Allah,
ba zan kuwa ɓoye daga gare ka ba;
21 Ka janye hannunka nesa da ni,
ka daina ba ni tsoro da bantsoronka.

22 Sa'an nan ka kira ni, zan kuwa amsa,
ko kuma ka bar ni in yi magana sai ka amsa mini.
23 Abubuwa nawa na yi waɗanda ba daidai ba, kuma zunubi ne?
Ka nuna mini laifina da zunubina.
24 Don me ka ɓoye mini fuskarka;
ka kuma sa na zama kamar maƙiyinka?
25 Ko za a wahalar da ganye wanda iska take hurawa?
Ko za ka bi busasshiyar ciyawa?
26 Gama ka rubuta abubuwa marasa daɗi game da ni;
ka sa na yi gādon zunuban ƙuruciyata.
27 Ka daure ƙafafuna da sarƙa;
kana kallon duk inda na taka
ta wurin sa shaida a tafin ƙafafuna.

28 "Haka mutum yake lalacewa kamar ruɓaɓɓen abu,
kamar rigar da asu ya cinye.

# 14

1 "Mutum haihuwar mace
kwanakinsa kaɗan ne, kuma cike da wahala.
2 Yana tasowa kamar fure yana kuma shuɗewa;
kamar inuwa, ba ya daɗewa.
3 Za ka zura ido a kan irin wannan ne?
Za ka kawo shi gaba don ka yi masa shari'a?
4 Wane ne zai iya kawo abin da yake da tsarki daga cikin abu marar tsarki?
Babu!
5 An lissafta kwanakin mutum;
ka riga ka ɗibar masa watanni,
ka yi masa iyaka, ba zai iya wuce iyakar ba.
6 Saboda haka ka kawar da kanka daga gare shi,
ka rabu da shi har sai ya cika lokacinsa kamar mutumin da aka ɗauki hayarsa.

7 "Aƙalla itace yana da bege.
In an sare shi, zai sāke tsira,
zai tohu da kyau.
8 Ko da jijiyoyin itacen sun tsufa a cikin ƙasa
kuma kututturensa ya mutu a cikin ƙasa.
9 Daga ya ji ƙanshin ruwa zai tohu
yă yi tsiro kamar shuka.
10 Amma mutum yana mutuwa a bizne shi;
daga ya ja numfashinsa na ƙarshe, shi ke nan.
11 Kamar yadda ruwa yake bushewa a teku ko a gaɓar rafi
sai wurin yă bushe,
12 haka mutum zai kwanta ba zai tashi ba;
har sai duniya ta shuɗe
mutane ba za su farka ba, ba za su tashi daga barcinsu ba.

13 "Da ma za ka ɓoye ni a cikin kabari
ka ɓoye ni har sai fushinka ya wuce!
In da za ka keɓe mini lokaci
sa'an nan ka tuna da ni!

14 In mutum ya mutu, ko zai sāke rayuwa?
In haka ne zan daure
kwanakin da nake shan wahala har su wuce.
15 Za ka kira zan kuwa amsa maka;
za ka yi marmarin abin da hannunka ya halitta.
16 Ba shakka a lokacin ne za ka lura da matakaina
amma ba za ka kula da zunubaina ba.
17 Za a daure laifofina a cikin jaka;
za ka rufe zunubaina.

18 "Amma kamar yadda manyan duwatsu suke fāɗuwa
su farfashe su kuma gusa daga wurarensu,
19 yadda ruwa yakan zaizaye duwatsu
ruwa mai ƙarfi kuma yă kwashe turɓayar ƙasa,
haka kake barin mutum ba bege.
20 Ka sha ƙarfinsa gaba ɗaya, sai ya ɓace,
ka sauya yanayinsa ka kuma kore shi.
21 Ko an martaba 'ya'yansa maza, ba zai sani ba;
Ko an wulaƙanta su, ba zai gani ba.
22 Zafin jikinsa kaɗai yake ji
yana kuka wa kansa ne kaɗai."

# 15

*Elifaz*

1 Sai Elifaz mutumin Teman ya amsa,
2 "Mutum mai hikima zai amsa da surutai marasa kan gado
ko yă cika cikinsa da iskar gabas?
3 Ko zai yi gardama da maganganun wofi
maganganu marasa amfani?
4 Amma ka ma rena Allah
ka hana a yi addu'a gare shi.
5 Zunubanka ne suke gaya maka abin da za ka ce;
kana magana kamar mai wayo.
6 Bakinka zai kai ka yă baro, ba nawa ba;
maganar bakinka za tă juya a kanka.

7 "Kai ne mutum na farko da aka fara haihuwa?
Ko kai ne aka fara halitta kafin tuddai?
8 Kana sauraron shawarar Allah?
Ko kana gani kai kaɗai ne mai hikima?
9 Me ka sani da ba mu sani ba?
Wane fahimi kake da shi da ba mu da shi?
10 Masu furfura da tsofaffi suna gefenmu
mutanen da sun girme babanka.
11 Ta'aziyyar Allah ba tă ishe ka ba.
Maganarsa mai laushi ba tă ishe ka ba?
12 Don me ka bar zuciyarka ta kwashe ka,
kuma don me idanunka suke haske,
13 har kake fushi da Allah
kake kuma faɗar waɗannan maganganu daga bakinka?

14 "Mene ne mutum, har da zai zama da tsarki,

ko kuma mace ta haife shi, har yă iya zama mai adalci?
15 In Allah bai nuna amincewa ga tsarkakansa ba,
in har sammai ba su da tsarki a idonsa,
16 mutum fa, wanda yake da mugunta da lalacewa,
wanda yake shan mugunta kamar ruwa!

17 “Ka saurare ni, zan kuma yi maka bayani;
bari in gaya maka abin da na gani,
18 abin da masu hikima suka ce,
ba tare da sun ɓoye wani abu da suka samu daga wurin iyayensu ba
19 (waɗanda su ne masu ƙasar
kafin baƙi su shigo ƙasar).
20 Dukan kwanakin ransa mugu yana shan wahala,
wahala kaɗai zai yi ta sha.
21 Kara mai bantsoro za tă cika kunnuwansa
ʼyan fashi za su kai masa hari.
22 Yana jin tsoron duhu
domin za a kashe shi da takobi.
23 Yana ta yawo, abinci don ungulaye;*
ya san ranar duhu tana kusa.
24 Ɓacin rai da baƙin ciki sun cika shi,
kamar sarkin da yake shirin yaƙi,
25 domin ya nuna wa Allah yatsa
ya rena Allah Maɗaukaki,
26 ya tasar masa da faɗa
da garkuwa mai kauri da kuma ƙarfi.

27 “Ko da yake fuskarsa ta cika da kumatu
kuma yana da tsoka koʼina,
28 zai yi gādon garuruwan da suka lalace,
da kuma gidajen da ba wanda yake zama a ciki,
gidajen da sun zama tarkace.
29 Ba zai sāke zama mai arziki ba, dukiyarsa ba za tă dawwama ba,
abin da ya mallaka kuma ba zai bazu a ƙasar ba.
30 Ba zai tsere wa duhu ba;
wuta za tă ƙona rassansa,
kuma numfashi daga bakin Allah zai hallaka shi.
31 Kada yă ruɗi kansa ta wurin dogara ga abin da ba shi da amfani
domin ba zai samu wani abu ba daga ciki.
32 Kafin lokacinsa yă cika, za a gama biyansa duka,
kuma rassansa ba za su ba da amfani ba.
33 Zai zama kamar itacen inabi wanda ʼyaʼyansa suka kakkaɓe kafin su nuna,
kamar itacen zaitun zai zubar da furensa.
34 Gama marasa tsoron Allah za su zama marasa ba da ʼyaʼya,
wuta kuma za tă ƙona tenti na masu son cin hanci.
35 Suna yin cikin rikici su kuma haifi mugunta;
cikinsu yana cike da ruɗami.”

# 16

*Ayuba*

* **15:23** Ko kuwa yawo, neman abinci

1 Sai Ayuba ya amsa,
2 “Na ji abubuwa da yawa kamar waɗannan;
dukanku ba ku iya ta’aziyya ba!
3 Dogayen surutanku ba sa ƙare ne?
Me yake sa kuke ta yin waɗannan surutai har kuke cin gaba da yin gardama?
4 Ni ma zan iya yin maganganu kamar yadda kuke yi
in da kuna cikin halin da nake;
zan iya faɗar duk abubuwan da kuke faɗi,
in kaɗa muku kaina.
5 Amma bakina zai ƙarfafa ku;
ta’aziyyar da za tă fito daga bakina za tă kawar muku da ɓacin zuciyarku.

6 “Duk da haka in na yi magana, ba na samun sauƙi;
in ma na yi shiru zafin ba ya tafiya.
7 Ba shakka ya Allah ka gajiyar da ni;
ka ɓata gidana gaba ɗaya.
8 Ka daure ni, ya kuma zama shaida;
yadda na rame sai ƙasusuwa, wannan ya sa ake gani kamar don ni mai zunubi ne shi ya sa.
9 Allah ya kai mini hari ya yi kaca-kaca da ni cikin fushinsa
yana cizon haƙoransa don fushin da yake yi da ni;
ya zura mini ido.
10 Mutane suka buɗe baki suka yi mini riyar reni;
suka yi mini ba’a
suka haɗu suka tayar mini.
11 Allah ya bashe ni ga mugayen mutane,
ya jefa ni hannun mugaye.
12 Dā ina zamana lafiya kome yana tafiya daidai;
amma ya ragargaza ni; ya shaƙe ni a wuya;
ya murƙushe ni na zama abin barata gare shi;
13 maharbansa sun kewaye ni.
Ba tausayi, ya soke ni a ƙodata
har jini ya zuba a ƙasa.
14 Ya ji mini rauni a kai a kai
ya auko mini kamar mai yaƙi.

15 “Ina makoki saye da tsummoki
na ɓoye fuskata a cikin ƙura.
16 Fuskata ta yi ja don kuka
idanuna sun kukumbura;
17 duk da haka hannuwana ba su aikata ɓarna ba
kuma addu’ata mai tsabta ce.

18 “Ya duniya, kada ki ɓoye jinina;
bari yă yi kuka a madadina!
19 Ko yanzu haka shaidata tana sama;
wanda zai tsaya mini yana sama.
20 Shi mai yin roƙo a madadina abokina ne
yayinda nake kuka ga Allah;
21 a madadin mutum ya yi roƙo ga Allah
kamar yadda mutum yakan yi roƙo domin abokinsa.

22 “Shekaru kaɗan suka rage
in kama hanyar da ba a komawa.

## 17

1 Na karaya,
kwanakina sun kusa ƙarewa,
kabari yana jirana.
2 Ba shakka masu yi mini ba’a suna kewaye da ni;
idanuna suna ganin tsokanar da suke yi mini.

3 “Ya Allah, ka ba ni abin da ka yi mini alkawari.
Wane ne zai kāre ni?
4 Ka rufe zuciyarsu yadda ba za su iya ganewa ba,
saboda haka ba za ka bari su yi nasara ba.
5 In mutum ya juya wa abokansa baya don a ba shi wata lada
’ya’yansa za su makance.

6 “Allah ya sa na zama abin da kowa yake magana a kai
wanda kowa yake tofa wa miyau a fuska.
7 Idanuna ba sa gani sosai don baƙin ciki;
jikina ya zama kamar inuwa kawai
8 Mutanen da suke masu adalci wannan abu ya ba su tsoro;
marasa laifi sun tayar wa marasa tsoron Allah.
9 Duk da haka, masu adalci za su ci gaba da tafiya a kan hanyarsu,
waɗanda hannuwansu suke da tsabta kuma za su ƙara ƙarfi.

10 “Amma ku zo dukanku, ku sāke gwadawa!
Ba zan sami mutum ɗaya mai hikima ba a cikinku.
11 Kwanakina sun wuce, shirye-shiryena sun ɓaci
haka kuma abubuwan da zuciyata take so.
12 Mutanen nan sun juya rana ta zama dare.
A tsakiyar duhu suka ce, ‘Haske yana kusa.’
13 In kabari ne begen da nake da shi kaɗai,
in na shimfiɗa gadona a cikin duhu,
14 In na ce wa kabari, ‘Kai ne mahaifina,’
tsutsa kuma ke ce, ‘Mahaifiyata’ ko ‘’yar’uwata,’
15 To, ina begena yake?
Wane ne zai iya ganin wani bege domina?
16 Ko begena zai tafi tare da ni zuwa kabari ne?
Ko tare za a bizne mu cikin ƙura?”

## 18

*Bildad*

1 Sai Bildad mutumin Shuwa ya amsa,
2 “Yaushe za ka gama maganganun nan?
Ka dawo da hankalinka sa’an nan za mu iya yin magana.
3 Don me muke kamar shanu a wurinka,
ka ɗauke mu mutanen wofi?
4 Kai da ka yayyage kanka don haushi,
za a yashe duniya saboda kai ne?
Ko kuma duwatsu za su matsa daga wurinsu?

5 “An kashe fitilar mugu;
harshen wutarsa ya daina ci.
6 Wutar cikin tentinsa ta zama duhu;
fitilar da take kusa da shi ta mutu.
7 Karfin takawarsa ya ragu;
dabararsa ta ja fāɗuwarsa.
8 Kafafunsa sun kai shi cikin raga,
yana ta yawo a cikin ragar.
9 Tarko ya kama ɗiɗɗigensa;
tarko ya riƙe shi kam.
10 An ɓoye masa igiya da za tă zarge shi a ƙasa;
an sa masa tarko a kan hanyar da zai bi.
11 Tsoro duk ya kewaye shi ta kowane gefe
yana bin shi duk inda ya je.
12 Masifa tana jiransa;
bala’i yana shirye yă fāɗa masa a lokacin da zai fāɗi.
13 Ya cinye wani sashe na gaɓar jikinsa;
ɗan fari na mutuwa ya cinye ƙafafunsa.
14 An yage shi daga zaman lafiyar da yake yi a cikin tentinsa
aka sa shi tsoro sosai.
15 Wuta ta cinye tentinsa;
farar wuta ta rufe wurin da yake zama.
16 Jijiyoyinsa sun bushe a ƙasa
rassansa sun mutu a sama.
17 An manta da shi a duniya;
ba wanda yake ƙara tunawa da shi.
18 An tura shi daga cikin haske zuwa cikin duhu,
an kore shi daga duniya.
19 Ba shi da ’ya’ya ko zuriya cikin mutanensa,
ba sauran wanda yake a raye a wurin da ya taɓa zama.
20 Mutanen Yamma suna mamakin abin da ya faru da shi;
tsoro ya kama mutanen gabas.
21 Ba shakka haka wurin zaman mugun mutum yake,
haka wurin zaman wanda bai san Allah ba yake.”

# 19

*Ayuba*

1 Sai Ayuba ya amsa,
2 “Har yaushe za ku yi ta ba ni azaba
ku kuma murƙushe ni da maganganunku?
3 Yanzu sau goma ke nan kuna wulaƙanta ni,
kuna kai mini hari na rashin kunya.
4 In gaskiya ne na yi laifi,
kuskurena ya rage nawa.
5 In kuwa za ku ɗaukaka kanku a kaina
kuna ɗauka wahalar da nake sha domin na yi laifi ne,
6 sai ku san cewa Allah ya yi mini ba daidai ba
ya kewaye ni da ragarsa.

7 “Ko da yake na yi kuka cewa, ‘An yi mini ba daidai ba!’ Ba a amsa mini ba;
ko da yake na nemi taimako, ba a yi adalci ba.

8 Ya tare mini hanya yadda ba zan iya wucewa ba;
ya rufe hanyata da duhu.
9 Ya cire darajar da nake da ita,
ya kuma cire rawani daga kaina.
10 Ya yi kaca-kaca da ni har sai da na ƙare;
ya tuge begen da nake da shi kamar itace.
11 Yana jin haushina
ya lissafta ni cikin maƙiyansa.
12 Rundunarsa ta zo da ƙarfi;
suka kafa sansani kewaye da ni,
suka zagaye tentina.

13 “Ya raba ni da ’yan’uwana maza;
abokaina sun zama baƙi gare ni.
14 Dangina sun tafi;
abokaina na kurkusa sun manta da ni.
15 Waɗanda sukan ziyarce ni,
da masu yi mini aiki mata sun ɗauke ni baƙo.
16 Na kira bawana, amma bai amsa ba,
ko da yake na roƙe shi da bakina.
17 Numfashina yana ɓata wa matata rai;
’yan’uwana sun ƙi ni.
18 Har ’yan yara suna rena ni;
in sun gan ni sai su fara yi mini riyar reni.
19 Duk abokaina sun yashe ni;
waɗanda nake ƙauna sun zama ba sa ƙaunata.
20 Ni ba kome ba ne sai dai fata da ƙashi,
da ƙyar na tsira.

21 “Ku tausaya mini, abokaina, ku ji tausayina,
gama hannun Allah ya sauko a kaina.
22 Don me kuke fafarata kamar yadda Allah yake yi?
Ba ku gaji da yagar fatata ba?

23 “Kash, da ma a ce ana rubuta maganganuna,
da an rubuta su a littafi,
24 a rubuta su da ƙarfe a kan dutse
don su dawwama har abada!
25 Na san wanda zai fanshe ni yana nan da rai,
kuma a ƙarshe zai tsaya a kan duniya.
26 Kuma bayan an hallaka fatata,
duk da haka a cikin jiki zan ga Allah.
27 Zan gan shi da kaina
da idanuna, Ni, ba wani ba ne.
Zuciyata ta cika da wannan tunani!

28 “In kuka ce, ‘Za ku ci gaba da matsa mini,
tun da shi ne tushen damuwa,’
29 sai ku ma ku ji tsoron takobin;
gama fushi yakan kawo hukunci ta wurin takobi,
sa’an nan za ku san cewa akwai shari’a.”

# 20

*Zofar*

1 Sai Zofar mutumin Na'ama ya amsa,
2 "Tunanin da ya dame ni ya sa dole in amsa
domin abin ya dame ni sosai.
3 Na ji wani zargin da ka yi mini na reni,
kuma yadda na gane, shi ya sa zan ba da amsa.

4 "Ba shakka ka san yadda abin yake tuntuni,
tun da aka sa mutum cikin duniya,
5 mugun mutum bai taɓa daɗewa ba,
farin cikin mutum na ɗan gajeren lokaci ne.
6 Ko da ya ƙasaita ya kai sararin sama,
kansa kuma yana taɓa gizagizai.
7 Zai hallaka har abada, kamar bayan gidansa;
waɗanda suka gan shi za su ce, 'Ina yake?'
8 Kamar mafarki haka zai ɓace, ba za a ƙara ganinsa ba
zai ɓace kamar wahayi da dare.
9 Idon da ya gan shi ba zai ƙara ganinsa ba;
wurin zamansa ba zai sāke ganinsa ba.
10 Dole 'ya'yansa su mayar wa matalauta abin da ya kamata;
dole hannuwansa su mayar da dukiyarsa.
11 Jin ƙarfi da ya cika ƙasusuwansa
zai kwantar da shi a cikin ƙura.

12 "Ko da yake mugunta tana da daɗi a bakinsa
kuma yana ɓoye ta a harshensa,
13 ko da yake ba zai iya rabuwa da ita ba,
yana kuma ajiye ta a bakinsa,
14 duk da haka abincin da ya ci zai zama da tsami a cikin cikinsa;
zai zama kamar dafin maciji a cikinsa.
15 Zai haras da dukiyar da ya haɗiye;
Allah zai sa cikinsa yǎ haras da su.
16 Zai sha dafin maciji;
sarar maciji mai dafi za tă tashe shi.
17 Ba zai ji daɗin koguna da rafuffuka
masu kwarara da zuma da madara ba.
18 Dole yǎ ba da abin da ya yi gumi kafin yǎ samu,
ba zai ci ba; ba zai ji daɗin ribar da ya samu daga kasuwancinsa ba.
19 Gama ya ci zalin talakawa ya bar su cikin wahala;
ya ƙwace gidajen da ba shi ya gina ba.

20 "Ba shakka ba zai samu abin da yake ƙoƙarin samu ba,
dukiyarsa ba za tă cece shi ba.
21 Ba abin da ya ragu da zai ɗauka;
arzikinsa ba zai dawwama ba.
22 Yana cikin samun arziki, ɓacin rai zai auka masa;
ƙunci mai ƙarfi zai zo masa.
23 Lokacin da ya cika cikinsa,
Allah zai zuba fushinsa a kansa,

zai daddaka shi.
24 Ko da yake yana guje wa makamin ƙarfe,
kibiya mai bakin tagulla za tă huda shi.
25 Zai zāre ta daga bayansa,
tsinin zai fita daga hantarsa;
tsoro zai cika shi;
26 duhu kawai yake jiran dukiyarsa.
Wutar da ba a fifita ba za tă cinye shi
ta kuma ƙona duk abin da ya rage a tentinsa.
27 Sammai za su fallasa laifinsa;
duniya za tă yi gāba da shi.
28 Ambaliyar ruwa za tă tafi da gidansa,
ruwaye masu gudu a ranar fushin Allah.
29 Abin da Allah zai sa yă faru da mugu ke nan,
gādon da Allah ya ba shi ke nan."

# 21

*Ayuba*

1 Sai Ayuba ya amsa,
2 "Ku saurare ni da kyau;
bari wannan yă zama ta'aziyyar da za ku ba ni.
3 Ku ba ni zarafi in yi magana,
bayan na gama sai ku yi ba'arku.

4 "A wurin mutum ne na kawo kukana?
Don me ba zan kāsa haƙuri ba?
5 Ku dube ni, ku kuma yi mamaki;
ku rufe bakina da hannunku.
6 Lokacin da na yi tunanin wannan,
sai in ji tsoro; jikina yă fara rawa.
7 Don me mugaye suke rayuwa har su tsufa,
suna kuma ƙaruwa da iko?
8 Suna ganin 'ya'yansu suna girma,
suna ganin jikokinsu suna tasowa a kan idanunsu.
9 Gidajensu suna zama cikin lafiya ba ruwansu da fargaba.
Kuma Allah ba ya ba su horo.
10 Shanunsu ba sa fasa haihuwa;
suna haihuwa ba sa yin ɓari.
11 Suna aika 'ya'yansu kamar garke;
'ya'yansu suna guje-guje da tsalle-tsalle.
12 Suna rera da kayan kiɗa na ganga da garaya;
suna jin daɗin busar sarewa.
13 Suna yin rayuwarsu cikin arziki
kuma su mutu cikin salama.
14 Duk da haka suna ce wa Allah, 'Ka rabu da mu.'
Ba ma so mu san hanyoyinka.
15 Wane ne Maɗaukaki har da za mu bauta masa?
Wace riba za mu samu ta wurin yin addu'a gare shi?
16 Amma arzikinsu ba a hannunsu yake ba
saboda haka ba ruwana da shawarar mugaye.

17 “Duk da haka, sau nawa fitilar mugu take mutuwa?
Sau nawa bala’i yake auka masa,
ko Allah ya taɓa hukunta mugu cikin fushi?
18 Sau nawa suke zama kamar tattaka a iska,
ko kuma kamar ƙura da iskar hadari take kwashewa?
19 An ce ‘Allah yana tara wa ’ya’yan mutum horon da zai ba mutumin.’
Bari yă ba mutumin horo don yă san ya yi haka!
20 Bari idanunsa su ga yadda zai hallaka;
bari yă sha daga fushin Maɗaukaki.
21 Ko zai damu da iyalin da ya bari a baya
sa’ad da kwanakinsa suka ƙare?

22 “Wani zai iya koya wa Allah ilimi
tun da yana shari’anta har da waɗanda suke manya masu iko?
23 Wani mutum zai mutu cikin jin daɗi
da kwanciyar hankali,
24 jikinsa ɓulɓul,
ƙasusuwansa da alamar ƙarfi.
25 Wani kuma zai mutu cikin ɗacin rai,
bai taɓa jin daɗin wani abu mai kyau ba.
26 Dukansu kuwa za a bizne su a ƙasa,
kuma tsutsotsi za su cinye su.

27 “Na san duk abin da kuke tunani,
yadda za ku saɓa mini.
28 Kuna cewa, ‘Yanzu ina gidan babban mutumin nan,
tenti wurin da mugaye suke zama?’
29 Ba ku taɓa tambayar waɗanda suke tafiya ba?
Ba ku kula da labaransu,
30 cewa an kāre mugu daga ranar bala’i,
an kāre shi daga ranar fushi?
31 Wane ne yake gaya masa abin da ya yi?
Wane ne yake rama abin da ya yi?
32 Za a bizne shi a kabari,
a kuma yi tsaron kabarinsa.
33 Akan mai da ƙasa a kan gawarsa a hankali;
dukan jama’a suna binsa,
da yawa kuma suna gabansa.

34 “Saboda haka ta yaya za ku iya yi mini ta’aziyya
da surutan banzan nan naku? Babu wani abu cikin amsarku sai ƙarya!”

# 22

*Elifaz*

1 Sai Elifaz mutumin Teman ya amsa,
2 “Mutum yana iya zama da amfani a wurin Allah?
Mai hikima ma zai iya zama da amfani a wurin shi?
3 Wane daɗi Allah zai ji in kai mai adalci ne?
Wace riba zai samu in rayuwarka marar laifi ce?

4 “Ko don kana tsoron Allah shi ya sa ya kwaɓe ka

ya kuma bari haka yă same ka?
5 Ba muguntarka ce ta yi yawa ba?
Ba zunubanka ne ba iyaka ba?
6 Ka sa ɗan'uwanka yă biya ka bashin da kake binsa ba dalili;
ka ƙwace wa mutanen rigunansu ka bar su tsirara.
7 Ba ka ba masu jin ƙishirwa su sha ba
kuma ka hana wa masu jin yunwa abinci su ci.
8 Ko da yake kai mai ƙarfi ne, ka mallaki ƙasa,
mutum mai martaba kuma, kana zama cikin ƙasarka.
9 Ka kori gwauraye hannu wofi,
ka kuma karya ƙarfin marayu.
10 Shi ya sa kake kewaye da tarkuna,
shi ya sa ka cika da tsoron mugun abin da zai auko maka.
11 An yi duhu ƙwarai, har ba ka iya gani,
shi ya sa ambaliyar ruwa ta rufe ka.

12 "Ba Allah ne a can sama ba?
Dubi yadda taurarin sama suke can nesa a sama!
13 Duk da haka ka ce, 'Me Allah ya sani?
A cikin duhu ne yake shari'a?
14 Gajimare ya rufe shi, saboda haka ba ya ganinmu
lokacin da yake takawa a cikin sammai.'
15 Za ka ci gaba da bin tsohuwar hanyar
da mugayen mutane suka bi?
16 An ɗauke su kafin lokacinsu yă cika,
ruwa ya share tushensu.
17 Suka ce wa Allah, 'Ka rabu da mu!
Me Maɗaukaki zai yi mana?'
18 Duk da haka kuwa shi ne ya cika gidajensu da abubuwa masu kyau,
saboda haka ba ruwana da shawarar mugaye.

19 "Masu adalci suna gani ana hallaka mugaye, suna jin daɗi;
marasa laifi suna yi musu ba'a, suna cewa,
20 'Ba shakka an hallaka maƙiyanmu,
wuta kuma ta ƙona dukiyarsu.'

21 "Ka miƙa kanka ga Allah ka samu salamarsa;
ta haka ne arziki zai zo maka.
22 Ka bi umarnin da zai fito daga bakinsa
kuma ka riƙe maganarsa a cikin zuciyarka.
23 In ka komo ga Maɗaukaki, za ka warke.
In ka kawar da mugunta daga cikin gidanka.
24 Ka jefar da zinariyarka a ƙasa,
ka jefar da zinariyar Ofir da ka fi so a cikin duwatsu,
25 sa'an nan ne Maɗaukaki zai zama zinariyarka,
zai zama azurfa mafi kyau a wurinka.
26 Ba shakka a lokacin ne za ka sami farin ciki
daga wurin Maɗaukaki,
ku kuma ɗaga idanunku ga Allah
27 Za ka yi addu'a zuwa gare shi, zai kuwa ji ka,
kuma za ka cika alkawuranka.

28 Abin da ka zaɓa za ka yi za ka yi nasara a ciki,
haske kuma zai haskaka hanyarka.
29 Sa'ad da aka ƙasƙantar da mutane ka kuma ce, 'A ɗaga su!'
Sa'an nan zai ceci masu tawali'u.
30 Zai ceci wanda ma yake mai laifi,
wanda zai tsirar da shi ta wurin tsabtar hannuwanka."

# 23

*Ayuba*

1 Sa'an nan Ayuba ya amsa,
2 "Ko a yau, ina kuka mai zafi;
hannunsa yana da nauyi duk da nishin da nake yi.
3 Da a ce na san inda zan same shi;
da a ce zan iya zuwa wurin da yake zama!
4 Zan kai damuwata wurinsa
in yi gardama da shi.
5 Zan nemi in san abin da zai ce mini,
in kuma auna abin da zai ce mini.
6 Zai yi gardama da ni da ikonsa mai girma?
Babu, ba zai zarge ni da laifi ba.
7 Mai adalci ne zai kawo ƙara a wurinsa,
kuma zan samu kuɓuta daga wurin mai shari'an nan har abada.

8 "Amma in na je gabas, ba ya wurin;
in na je yamma, ba zan same shi ba.
9 Sa'ad da yake aiki a arewa, ba ni ganinsa;
sa'ad da ya juya zuwa kudu, ba na ganinsa.
10 Amma ya san hanyar da nake bi;
sa'ad da ya gwada ni zan fito kamar zinariya.
11 Kafafuna suna bin ƙafafunsa kurkusa;
na bi hanyarsa ba tare da na juya ba.
12 Ban fasa bin dokokin da ya bayar ba;
na riƙe maganarsa da muhimmanci fiye da abincin yau da gobe.

13 "Amma ya tsaya shi kaɗai, kuma wa ya isa yă ja da shi?
Yana yin abin da yake so.
14 Yana yi mini abin da ya shirya yă yi mini,
kuma yana da sauran irinsu a ajiye.
15 Shi ya sa na tsorata a gabansa;
sa'ad da na yi tunanin wannan duka, nakan ji tsoronsa.
16 Allah ya sa zuciyata ta yi sanyi;
Maɗaukaki ya tsorata ni.
17 Duk da haka duhun bai sa in yi shiru ba,
duhun da ya rufe mini fuska.

# 24

1 "Domin me Maɗaukaki ba zai sa ranar shari'a ba?
Don me waɗanda suka san shi suke faman samun irin ranakun nan?
2 Mugaye suna satar fili ta wurin matsar da duwatsun da aka yi iyaka da su;
suna satar dabbobi su kuma yi kiwon su.

3 Suna ƙwace wa marayu jakunansu
suna kuma ƙwace wa gwauruwa sa don suna binta bashi.
4 Suna ture matalauta daga hanya
suna kuma sa dole matalautan ƙasar su ɓoye.
5 Kamar jakunan jeji a hamada,
matalauta suna aikin neman abinci
gonaki marasa amfani suna tanada abinci wa ʼyaʼyansu.
6 Suna girbi a gonakin da ba nasu ba,
suna yin kala a gonar inabi ta mugaye.
7 Don ba su da tufafi, sukan kwana tsirara;
ba su da wani abin da zai rufe su cikin sanyi.
8 Sun jiƙe sharkaf da ruwan da yake kwararowa daga duwatsu,
sun rungume duwatsu don rashin wurin fakewa.
9 Ana ƙwace jinjiri mai shan mama;
ana ƙwace ɗan yaron matalauci don biyan bashi.
10 Don ba su da tufafi suna yawo tsirara;
suna dakon dammunan hatsi
amma duk da haka suna cikin shan yunwa.
11 Suna matse zaitun a cikin kunyoyi
suna kuma matse ruwan inabi daga ʼyaʼyan inabi, duk da haka suna fama da ƙishi.
12 Ana jin nishin masu mutuwa daga birni,
kuma rayukan waɗanda aka ji musu rauni suna kuka suna kira don taimako.
Amma bai ba wani laifi ba.

13 "Akwai waɗanda suke yi wa haske tawaye,
waɗanda ba su san hanyoyinsa ba
ko kuma ba su taɓa bin hanyoyinsa ba.
14 Saʼad da hasken yini ya tafi, mai kisankai yakan tashi;
yǎ je yǎ kashe matalauta da masu bukata;
a cikin dare yake shigowa kamar ɓarawo.
15 Idanun mazinaci suna jiran yamma ta yi sosai;
yana tunani cewa, 'Ba wanda zai gan ni,'
sai kuma yǎ ɓoye fuskarsa.
16 Cikin duhu mutane suna fasa gidaje,
amma da rana sukan kulle kansu;
ba sa so wani abu yǎ haɗa su da haske.
17 Gama dukansu, duhu mai yawa shi ne safiyarsu;
suna abokantaka da razanar duhu.

18 "Duk da haka kamar abu marar nauyi suke a kan ruwa;
gefen ƙasar da suke, an laʼanta ta,
yadda ba wanda yake zuwa gonar inabinsu.
19 Kamar yadda zafi da fǎri suke shanye ƙanƙarar da ta narke,
haka kabari zai ƙwace waɗanda suka yi zunubi.
20 Waɗanda suka haife su za su manta da su,
tsutsotsi za su cinye su;
ba za a sāke tunawa da mugaye ba
amma an sare su kamar itace.
21 Suna cutar macen da ba ta da ɗa,
suna nuna wa gwauruwa rashin alheri.

22 Amma Allah cikin ikonsa yakan kawar da masu ƙarfi,
ko da yake sun yi ƙarfi, ba su da tabbacin rayuwa.
23 Mai yiwuwa zai bar su su zauna cikin kwanciyar hankali,
amma idanunsa suna kansu.
24 Sukan samu cin nasara na ɗan lokaci,
amma kuma za su ɓace; za su fāɗi
a tattara su kamar sauran; za a datse su kamar kan hatsi.

25 "In wannan ba haka ba ne,
wane ne zai shaida ƙarya nake yi har yă ƙi yarda da maganata?"

# 25

*Bildad*

1 Sai Bildad mutumin Shuwa ya amsa,
2 "Mulki na Allah ne, dole a ji tsoronsa;
yana tafiyar da kome yadda ya kamata a cikin sama.
3 Za a iya ƙirga rundunarsa?
A kan wane ne ba ya haska haskensa?
4 Ta yaya mutum zai iya zama mai adalci a gaban Allah?
Ta yaya mutumin da mace ta haifa zai zama mai tsarki?
5 In har wata da taurari
ba su da tsarki a idanunsa,
6 mutum fa? Ai, wannan tsutsa ne, ɗan ƙwaro kawai.
Me mutum ya daɗa a gaban Allah!"

# 26

*Ayuba*

1 Sai Ayuba ya amsa,
2 "Yadda ka taimaki marar ƙarfi!
Yadda ka ceci marar ƙarfi!
3 Ka ba marar hikima shawara!
Ka nuna kana da ilimi sosai.
4 Wane ne ya taimake ka ka yi waɗannan maganganu?
Kuma ruhun wane ne ya yi magana ta bakinka?

5 "Matattu suna cikin azaba, waɗanda suke ƙarƙashin ruwaye
da dukan mazauna cikin ruwaye.
6 Mutuwa tsirara take a gaban Allah;
haka kuma hallaka take a buɗe.
7 Ya shimfiɗa arewancin sararin sama a sarari;
ya rataye duniya ba a jikin wani abu ba.
8 Ya naɗe ruwaye a cikin gizagizansa,
duk da haka girgijen bai yage saboda nauyi ba.
9 Ya rufe fuskar wata,
ya shimfiɗa gizagizai a kan shi,
10 ya zāna iyakar fuskar ruwa
a kan iyakar da take tsakanin duhu da haske.
11 Madogaran sama sun girgiza,
saboda tsawatawarsa.
12 Da ikonsa ya kwantar da teku;
da hikimarsa ya hallaka dodon ruwan nan Rahab.
13 Da numfashinsa ya sa sararin sama ya yi kyau

da hannunsa ya soke macijin nan mai gudu.
14 Waɗannan kaɗan ke nan daga cikin ayyukansa masu yawa.
Kaɗan kawai muke ji game da shi!
Wane ne kuwa yake iya gane tsawar ikonsa?"

# 27

1 Ayuba kuwa ya ci gaba da magana,
2 "Na rantse da Allah mai rai, wanda ya danne mini gaskiyata,
Maɗaukaki, wanda ya sa nake cikin ɗacin rai.
3 Muddin ina da rai a cikina
kuma numfashin Allah yana cikin hancina,
4 bakina ba zai faɗi mugun abu ba,
harshena kuma ba zai yi ƙarya ba.
5 Ba zan taɓa yarda cewa kuna da gaskiya ba;
har in mutu, ba zan daina kāre mutuncina ba.
6 Zan ci gaba da adalcina, ba zan fasa ba;
lamirina ba zai taɓa yashe ni ba, dukan kwanakin raina.

7 "Bari maƙiyana su zama kamar mugaye,
masu gāba da ni kuma su zama kamar marasa adalci.
8 Gama wane bege marar tsoron Allah yake da shi,
lokacin da aka datse shi, lokacin da Allah ya ɗauke ransa?
9 Ko Allah yana sauraron kukansa
lokacin da ƙunci ya auko masa?
10 Ko zai sami farin ciki daga Maɗaukaki?
Ko zai yi kira ga Allah a kowane lokaci?

11 "Zan koya muku game da ikon Allah;
ba zan ɓoye hanyoyin Maɗaukaki ba.
12 Duk kun ga wannan ku da kanku
saboda haka me ya sa kuke maganganun nan marasa ma'ana?

13 "Ga abin da mugaye za su samu
gādon da azzalumi zai samu daga Maɗaukaki.
14 Kome yawan 'ya'yansa, takobi za tă gama da su;
zuriyarsa ba za su taɓa samun isashen abinci ba.
15 Waɗanda suka tsira annoba za tă kashe su,
kuma gwaurayensu ba za su yi kukan mutuwarsu ba.
16 Ko da yake ya tara azurfa kamar ƙasa,
tufafi kuma kamar tarin ƙasa,
17 abin da ya tara masu adalci za su sa
marasa laifi za su raba azurfarsa.
18 Gidan da ya gina kamar gidan gizo-gizo,
kamar bukkar mai tsaro.
19 Attajiri zai kwanta, amma daga wannan shi ke nan;
lokacin da zai buɗe idanunsa, kome ya tafi.
20 Tsoro zai kwashe shi kamar ambaliyar ruwa;
Da dare iska za tă tafi da shi.
21 Iskar gabas za tă tafi da shi; shi ke nan ya ƙare;
za tă share shi daga wurinsa.
22 Za tă murɗe shi ba tausayi,

lokacin da yake guje wa ikon iskar.
23 Zai tafa hannu yă yi tsaki
yă kawar da shi daga wurinsa."

# 28

1 Akwai ramin azurfa
akwai kuma wurin da ake tace zinariya.
2 Daga cikin ƙasa ake ciro ƙarfe,
ana kuma narkar da tagulla daga cikin dutse.
3 Mutum ya kawo ƙarshen duhu;
yakan bincike zuzzurfar iyaka,
yana neman duwatsu a wuri mafi duhu.
4 Nesa da inda mutane suke zama,
yakan huda rami yă yi abin lilo,
a wurin da mutane ba sa bi.
5 Cikin ƙasa inda ake samun abinci,
a ƙarƙashinta kuwa zafi ne kamar wuta;
6 akwai duwatsu masu daraja a cikin duwatsunta,
akwai kuma zinariya a cikin ƙurarta.
7 Tsuntsu mai farauta bai san hanyarta ba,
ba shahon da ya taɓa ganin ta.
8 Manyan namun jeji ba su taɓa binta ba,
ba zakin da ya taɓa binta.
9 Hannun mutum ya iya sarrafa ƙanƙarar duwatsu,
yă kuma tumɓuke tushen duwatsu.
10 Yana tona rami a cikin duwatsu
idanunsa suna ganin dukan dukiyar da ke cikin duwatsun.
11 Yana nema daga ina ruwan rafi yake ɓulɓulowa
yana kuma binciko abubuwan da suke a ɓoye yă kawo su cikin haske.

12 Amma a ina ne za a iya samun hikima?
Ina fahimta take zama?
13 Mutum bai gane muhimmancinta ba,
ba a samunta a ƙasar masu rai.
14 Zurfi ya ce, "Ba ta wurina";
teku ya ce, "Ba ta wurina."
15 Ba irin zinariyar da za tă iya sayenta,
ko kuma a iya auna nauyinta da azurfa.
16 Ba za a iya sayenta da zinariyar Ofir,
ko sauran duwatsu masu daraja ba.
17 Zinariya da madubi ba za su iya gwada kansu da ita ba,
ba kuwa za a iya musayarta da abubuwan da aka yi da zinariya ba.
18 Kada ma a ce murjani da duwatsu masu walƙiya;
farashin hikima ya fi na lu'ulu'ai.
19 Ba za a iya daidaita darajarta da duwatsun Tofaz na Kush ba,
zallar zinariya ma ba tă isa ta saye ta ba.

20 "To, daga ina ke nan hikima ta fito?
Ina fahimta take zama?
21 An ɓoye ta daga idanun kowane abu mai rai,

har tsuntsayen sararin sama ma an ɓoye masu ita.
22 Hallaka da mutuwa suna cewa,
'Jita-jitarta kaɗai muke ji.'
23 Allah ya gane hanyar zuwa wurinta.
Shi ne kaɗai ya san inda take zama,
24 Gama yana ganin iyakar duniya
kuma yana ganin duk abin da yake ƙarƙashin sama.
25 Lokacin da ya yi iska ya sa ta hura,
ya kuma auna ruwaye.
26 Lokacin da ya yi wa ruwan sama doka
da kuma hanya domin walƙiya,
27 sai ya dubi hikima ya auna ta;
ya tabbatar da ita, ya gwada ta.
28 Ya kuma ce wa mutum,
'Tsoron UBANGIJI shi ne hikima,
kuma guje wa mugunta shi ne fahimi.' "

# 29

1 Ayuba ya ci gaba da jawabinsa,
2 "Da ma ina nan lokacin da ya wuce baya can,
kwanakin da Allah yake lura da ni,
3 lokacin da fitilarsa take haske a kaina
na yi tafiya cikin duhu tare da haskensa.
4 Kwanakin da nake tasowa,
lokacin da abokantakar Allah ta sa wa gidana albarka,
5 lokacin da Maɗaukaki yana tare da ni,
kuma 'ya'yana suna kewaye da ni,
6 lokacin da ake zuba madara a inda nake takawa,
duwatsu kuma suna ɓulɓulo mini man zaitun.

7 "Sa'ad da na je ƙofar birni na zauna
a bainin jama'a,
8 matasan da suka gan ni sukan ja gefe
tsofaffi kuma suka tashi tsaye;
9 sarakuna suka yi shiru
suka rufe bakunansu da hannuwansu;
10 Muryar manya ta yi tsit
harshensu ya manne a rufin bakunansu.
11 Duk wanda ya ji ni ya yaba mini
waɗanda suka gan ni kuma sun amince da ni,
12 domin na ceci matalauta waɗanda suka nemi taimako,
da marasa mahaifi waɗanda ba su da wanda zai taimake su.
13 Mutumin da yake bakin mutuwa ya sa mini albarka.
Na faranta wa gwauruwa zuciya.
14 Na yafa adalci ya zama suturata;
gaskiya ita ce rigata da rawanina.
15 Ni ne idon makafi
kuma ƙafa ga guragu.
16 Ni mahaifi ne ga masu bukata;
na tsaya wa baƙo.
17 Na karya ƙarfin mugaye

na ƙwato waɗanda suke riƙe da haƙoransu.

18 “Na yi tunani cewa, ‘Zan mutu a cikin gidana,
kwanakina da yawa kamar turɓayar ƙasa.
19 Jijiyoyina za su kai cikin ruwa,
kuma raɓa za tă kwanta a rassana dukan dare.
20 Ɗaukakata za tă kasance tare da ni garau,
bakana koyaushe sabo ne a hannuna.’

21 “Mutane suna mai da hankali su saurare ni,
suna yin shiru don su ji shawarata.
22 Bayan da na yi magana, ba su ƙara ce kome ba.
Maganata ta shige su.
23 Sukan jira ni kamar yadda ake jiran ruwan sama.
Sukan sha daga cikin maganganuna kamar mai shan ruwan bazara.
24 Sa’ad da na yi musu murmushi da ƙyar sukan yarda;
hasken fuskata yana da daraja a gare su.
25 Na zaɓar masu inda za su bi na kuma zauna kamar sarkinsu;
na zauna kamar sarki a cikin rundunansu;
ina nan kamar mai yi wa masu makoki ta’aziyya.

# 30

1 “Amma yanzu suna yi mini ba’a
waɗanda na girme su,
waɗanda iyayensu maza ba su isa
su zama karnukan kiwon garken tumakina ba.
2 Ina amfani ƙarfin hannuwansu gare ni,
tun da ba su da sauran kuzari?
3 Duk sun rame don rashi da yunwa,
suna yawo a gaigayar ƙasa
a kufai da dare.
4 A cikin jeji suna tsinkar ganyaye marasa daɗi,
jijiyoyin itacen kwakwa ne abincinsu.
5 An kore su daga cikin mutanensu,
aka yi musu ihu kamar ɓarayi.
6 An sa dole su zauna a kwazazzabai da kuma
cikin kogunan duwatsu da kuma cikin ramummuka cikin ƙasa.
7 Suka yi ta kuka kamar dabbobi a jeji,
suka taru a ƙarƙashin sarƙaƙƙiya.
8 Mutane marasa hankali marasa suna,
an kore su daga ƙasar.

9 “Yanzu kuma ’ya’yansu maza su suke yi mini ba’a cikin waƙa
na zama abin banza a gare su.
10 Suna ƙyamata suna guduna;
suna tofa mini miyau a fuska.
11 Yanzu da Allah ya kunce bakana ya ba ni wahala
sun raba ni da mutuncina.
12 A hannun damana ’yan tā-da-na-zaune-tsaye sun tayar;
sun sa tarko a ƙafafuna,
sun yi shirin hallaka ni.

13 Sun ɓata mini hanyata;
sun yi nasara cikin hallaka ni,
ba tare da wani ya taimake su ba.
14 Suka nufo ni daga kowane gefe;
suka auko mini da dukan ƙarfinsu.
15 Tsoro ya rufe ni;
an kawar mini mutuncina kamar da iska,
dukiyata ta watse kamar girgije.

16 “Yanzu raina yana ƙarewa;
kwanakin wahala sun kama ni.
17 Dare ya huda ƙasusuwana;
ina ta shan azaba ba hutawa.
18 A cikin girman ikonsa Allah ya zama kamar riga a jikina;
ya shaƙe ni kamar wuyan rigata.
19 Ya jefa ni cikin laka,
na zama ba kome ba sai ƙura da toka.

20 “Na yi kuka gare ka ya Allah, amma ba ka amsa mini ba.
Na tashi tsaye, amma sai ka dube ni kawai.
21 Ka dube ni ba tausayi;
Ka kai mini hari da ƙarfin hannunka.
22 Ka ɗaga ni sama ka ɗora ni a kan iska;
ka jujjuya ni cikin hadari.
23 Na san za ka sauko da ni ga mutuwa
zuwa wurin da kowane mai rai zai je.

24 “Ba shakka ba mai ɗora hannu a kan mutumin da yake cikin wahala.
Lokacin da ya yi kukan neman taimako a cikin wahalarsa.
25 Ashe ban yi kuka domin waɗanda suke cikin damuwa ba?
Ko zuciyata ba tă yi baƙin ciki domin matalauta ba?
26 Duk da haka sa’ad da nake begen abu mai kyau,
mugun abu ne ya zo;
Sa’ad da nake neman haske, sai duhu ya zo.
27 Zuciyata ba tă daina ƙuna ba;
ina fuskantar kwanakin wahala.
28 Na yi baƙi ƙirin, amma ba rana ce ta ƙona ni ba.
Na tsaya a cikin mutane, na kuma yi kuka don taimako.
29 Na zama ɗan’uwan diloli,
na zama abokan mujiyoyi.
30 Fatar jikina ta yi baƙi tana ɓarewa;
jikina yana ƙuna da zazzaɓi.
31 Garayata ta zama ta makoki,
sarewata kuma ta zama ta kuka.

# 31

1 “Na yi alkawari da idanuna
kada su dubi budurwa da muguwar sha’awa.
2 Gama mene ne rabon mutum daga Allah a sama,
gādonsa daga Maɗaukaki a sama?
3 Ba masifa ba ne domin mugaye,

hallaka kuma ga waɗanda suka yi ba daidai ba?
4 Bai ga hanyoyina ba ne
bai ƙirga kowace takawata ba?

5 “In da na yi tafiya cikin rashin gaskiya
ko kuma ƙafata ta yi sauri zuwa yin ƙarya,
6 Bari Allah yă auna a kan ma’auni na gaskiya
zai kuma san cewa ni marar laifi ne.
7 In takawata ta kauce daga hanya,
in zuciyata ta bi abin da idanuna ke so,
ko kuma in hannuwana suna da laifi;
8 bari waɗansu su ci abin da na shuka,
kuma bari a tuge amfanin gonata.

9 “In sha’awar mace ya shiga mini zuciya,
ko kuma na laɓe a ƙofar maƙwabcina,
10 sai matata ta niƙa hatsin wani
kuma waɗansu maza su kwana da ita.
11 Gama wannan zai zama abin kunya,
zunubin da za a yi shari’a a kai.
12 Wuta ce take ƙuna har ta hallakar;
za tă cinye saiwar abin da na shuka ƙurmus.

13 “In da na danne wa bayina maza da mata hakkinsu,
sa’ad da suke da damuwa da ni,
14 me zan yi lokacin da Allah ya tuhume ni?
Me zan ce lokacin da ya tambaye ni?
15 Shi wanda ya yi ni a cikin uwata ba shi ne ya yi su ba?
Ba shi ne ya yi mu a cikin uwayenmu ba?

16 “In na hana wa matalauta abin da suke so,
ko kuma in sa idanun gwauruwa su yi nauyi don kuka,
17 in na ajiye burodina don kaina kaɗai,
ban kuwa ba wa marayu abinci sa’ad da suke jin yunwa,
18 amma tun suna tasowa na lura da su,
kamar yadda mahaifi zai lura da ɗa, kuma tun da aka haife ni ina lura da gwauruwa.
19 In da na ga wani yana mutuwa don rashin sutura,
ko wani mai bukata da ba shi da riga,
20 kuma zuciyarsa ba tă gode mini ba
don na yi masa sutura da gashin tumakina,
21 in na ɗaga hannuna don in cuci maraya,
domin na san in na faɗa za a ji ni a wurin masu shari’a,
22 bari hannuna yă guntule daga kafaɗata,
bari yă tsinke daga inda aka haɗa shi.
23 Gama ina jin tsoron hallaka daga Allah,
kuma domin tsoron ɗaukakarsa ba zan iya yin waɗannan abubuwa ba.

24 “In na dogara ga zinariya
ko kuma na ce wa zallan zinariya, ‘Gare ki nake dogara,’
25 in na yi fahariya don yawan dukiyata,

arzikin da hannuwana suka samu.
26 In na dubi rana cikin haskenta,
ko kuma wata yana tafiyarsa,
27 zuciyata ta jarrabtu gare su a ɓoye,
hannuna kuma ya sumbace su.
28 Waɗannan ma za su zama zunubin da za a shari'anta ke nan
don zai zama na yi wa Allah na sama rashin aminci.

29 "In na yi murna domin mugun abu ya faru da maƙiyina;
ko kuma domin wahala ta same shi,
30 ban bar bakina yă yi zunubi
ta wurin la'anta shi ba,
31 in mutanen gidana ba su taɓa cewa,
'Wane ne bai ƙoshi da naman Ayuba ba?'
32 Ba baƙon da ya taɓa kwana a titi,
gama koyaushe ƙofata tana buɗe domin matafiya,
33 in na ɓoye zunubina yadda mutane* suke yi,
ta wurin ɓoye laifina a cikin zuciyata,
34 domin ina tsoron taron mutane
kuma ina tsoron wulaƙancin da dangina za su yi mini,
sai na yi shiru kuma ban fita waje ba.

35 ("Kash, da ina da wanda zai ji ni!
Na sa hannu ga abin da na faɗa don kāre kaina,
bari Maɗaukaki yă amsa mini; bari mai tuhumata da laifi yă yi ƙarata a rubuce.
36 Ba shakka sai in ɗora a kafaɗata,
zan aza a kaina kamar rawani.
37 Zan ba shi lissafin duk abin da na taɓa yi;
zan zo gabansa kamar ɗan sarki.)

38 "In ƙasata tana kuka da ni
kunyoyinta duk sun cika da hawaye,
39 in na kwashe amfaninta ban biya ba
ko kuma na kashe masu ita,
40 bari ƙaya ta fito a maimakon alkama
ciyawa kuma a maimakon sha'ir."
Maganar Ayuba ta ƙare.

# 32

*Elihu*

1 Sai mutanen nan uku suka daina amsa wa Ayuba, domin a ganinsa shi mai adalci
ne. 2 Amma Elihu ɗan Barakel mutumin Buz na iyalin Ram, ya ji haushi da Ayuba don
yă nuna shi ne mai gaskiya ba Allah ba. 3 Ya kuma ji haushin abokan nan guda uku,
don sun kāsa amsa wa Ayuba ko da yake sun nuna Ayuba ne yake da laifi. 4 Elihu ya
jira sai a wannan lokaci ne ya yi magana da Ayuba, don shi ne yaro a cikinsu duka.
5 Amma sa'ad da Elihu ya ga mutanen nan uku ba su da abin cewa, sai ya fusata.
6 Sai Elihu ɗan Barakel mutumin Buz ya ce,
"Ni ƙarami ne a shekaru,
ku kuma kun girme ni;

* 31:33 Ko kuwa yadda Adamu ya yi

shi ya sa na ji tsoro
na kāsa gaya muku abin da na sani.
7 Na ɗauka ya kamata 'shekaru su yi magana;
ya kamata yawan shekaru su koyar da hikima.'
8 Amma ruhun da yake cikin mutum,
numfashin Maɗaukaki shi ne yake ba shi ganewa.
9 Ba tsofaffi ne kaɗai suke da hikima ba,
ba masu yawan shekaru ne suke gane abin da yake daidai ba.

10 "Saboda haka nake ce muku, ku saurare ni;
ni ma zan gaya muku abin da na sani.
11 Na jira sa'ad da kuke magana,
na ji muhawwararku
lokacin da kuke neman abin da za ku faɗa,
12 na saurare ku da kyau.
Amma ba waninku da ya nuna Ayuba yana da laifi;
ba ko ɗayanku da ya amsa muhawwararsa.
13 Kada ku ce, 'Mun sami hikima;
Allah ne kaɗai yake da ikon yin nasara da shi ba mutum ba.'
14 Amma ba da ni Ayuba ya yi gardama ba
kuma ba zan amsa masa da irin amsarku ba.

15 "Mamaki ya kama su kuma ba su da abin cewa;
kalmomi sun kāsa musu.
16 Dole ne in jira yanzu da suka yi shiru,
yanzu da suke tsaye a wurin ba su da amsa.
17 Ni ma zan faɗi nawa;
ni ma zan faɗi abin da na sani.
18 Gama ina cike da magana,
kuma ruhun da yake cikina yana iza ni;
19 a ciki ina kamar ruwan inabi wanda aka rufe a cikin kwalaba,
kamar sabuwar salkar ruwan inabi mai shirin fashewa.
20 Dole in yi magana in sami lafiya;
dole in buɗe baki in ba da amsa.
21 Ba zan nuna wa wani sonkai ba,
ko kuma in yi wa wani daɗin baki ba;
22 gama da a ce na iya daɗin baki,
da wanda ya yi ni ya ɗauke ni daga nan tuntuni.

# 33

1 "Amma yanzu, Ayuba, ka saurari abin da zan ce;
ka sa hankali ga kowane abin da zan faɗa.
2 Zan yi magana;
kalmomina suna dab da fitowa daga bakina.
3 Abin da zan faɗa gaskiya ne daga cikin zuciyata;
bakina zai faɗi gaskiyar abin da na sani.
4 Ruhun Allah ne ya yi ni;
numfashin Maɗaukaki ya ba ni rai.
5 Ka amsa mini in za ka iya;
ka yi shirin fuskanta ta.
6 Ni kamar ka nake a gaban Allah;

ni ma daga ƙasa aka yi ni.
7 Kada ka ji tsorona,
ba abin da zai fi ƙarfinka.

8 “Amma ka faɗa na ji,
na ji daidai abin da ka faɗa,
9 ‘ni mai tsarki ne marar zunubi;
ina da tsabta kuma ba ni da laifi.
10 Duk da haka Allah ya same ni da laifi;
ya ɗauke ni maƙiyinsa,
11 ya daure ƙafafuna da sarƙa;
yana tsaron duk inda na bi.’

12 “Amma na gaya maka, a nan ba ka yi daidai ba,
gama Allah ya fi mutum girma.
13 Don me ka yi masa gunaguni
cewa ba ya amsa tambayoyin mutum?
14 Gama Allah yana magana,
yanzu ga wannan hanya, yanzu kuma ga wata hanya
ko da yake ba lalle mutum yă lura ba.
15 A cikin mafarki, cikin wahayi da dare,
sa’ad da barci mai zurfi ya fāɗo a kan mutane
lokacin da suke cikin barci kan gadajensu,
16 mai yiwuwa yă yi musu magana a cikin kunnuwansu
yă razana su da gargaɗinsa,
17 don a juyar da su daga abin da yake yi da ba daidai ba
a kuma hana su daga girman kai,
18 don a kāre su daga fāɗuwa cikin rami,
a kāre su daga hallaka ta wurin takobi.

19 “Ko kuma mutum yă sha horo
ta wurin kwanciya da ciwo da rashin jin daɗi cikin ƙasusuwansa,
20 yadda zai ji ƙyamar abinci,
har yă ƙi son abinci mafi daɗi.
21 Naman jikinsa ya lalace ba wani abu mai kyau a ciki
kuma ƙasusuwansa da suke a rufe da tsoka yanzu duk sun fito.
22 Ransa yana matsawa kusa da rami,
ransa kuma kusa da ’yan aikan mutuwa.
23 Duk da haka, in akwai mala’ika a gefensa kamar matsakanci,
ɗaya daga cikin dubu,
da zai gaya wa mutum abin da yake daidai gare shi,
24 yă yi masa alheri yă ce,
‘Kada ka bari yă fāɗa cikin rami,
na samu fansa dominsa.’
25 Sa’an nan fatar jikinsa za tă zama sabuwa kamar ta jariri;
za tă zama kamar lokacin da yake matashi.
26 Ya yi addu’a ga Allah ya kuwa samu alheri a wurinsa,
yana ganin fuskar Allah yana kuma yin sowa don murna;
Allah ya mayar da shi ya zama mai adalci.
27 Sa’an nan sai ya zo wurin, wurin mutane ya ce,
‘Na yi zunubi, na kauce wa abin da yake daidai,

amma ban samu abin da ya kamata in samu ba.
28 Ya fanshi raina daga fāɗawa cikin rami,
kuma zan rayu in ji daɗin hasken.'

29 "Allah ya yi wa mutum duk waɗannan,
sau biyu, har ma sau uku.
30 Ya juyo da ransa daga fāɗawa cikin rami,
don hasken rai ya haskaka a kansa.

31 "Ka sa hankali da kyau, Ayuba, ka saurare ni;
ka yi shiru zan yi magana.
32 In kana da abin da za ka ce, ka amsa mini;
yi magana, domin ina so in 'yantar da kai.
33 Amma in ba haka ba, sai ka saurare ni;
yi shiru, zan kuma koya maka hikima."

# 34

1 Sa'an nan Elihu ya ce,
2 "Ku ji maganata, ku masu hikima;
ku saurare ni, ku masu ilimi.
3 Gama kunne yana rarrabe magana
kamar yadda harshe yake ɗanɗana abinci.
4 Bari mu zaɓi abin da yake daidai,
bari mu koyi abin da yake mai kyau tare.

5 "Ayuba ya ce, 'Ba ni da laifi,
amma Allah ya hana mini hakkina.
6 Ko da yake ina da gaskiya,
an ɗauke ni maƙaryaci;
ko da yake ba ni da laifi,
kibiyoyinsa sun ji mini ciwo wanda ba ya warkewa.'
7 Wane mutum ne kamar Ayuba,
wanda yake shan ba'a kamar ruwa?
8 Yana abokantaka da masu aikata mugunta;
yana cuɗanya da mugaye.
9 Gama ya ce, 'Ba ribar da mutum zai samu
lokacin da yake ƙoƙari yă faranta wa Allah zuciya.'

10 "Saboda haka ku saurare ni, ku masu ganewa.
Ko kaɗan Allah ba ya mugunta,
Maɗaukaki ba ya kuskure.
11 Yana biyan mutum bisa ga abin da ya yi;
yana kawo masa abin da ayyukansa suka jawo.
12 Ba zai yiwu Allah yă yi ba daidai ba,
Maɗaukaki ba zai yi shari'a marar gaskiya ba.
13 Wane ne ya ba shi iko yă lura da duniya?
Wane ne ya ba shi iko kan dukan duniya?
14 In nufinsa ne
ya kuma janye ruhunsa da numfashinsa,
15 'yan adam duka za su hallaka tare,
mutum kuma zai koma ƙasa.

16 “In kana da ganewa sai ka saurari wannan;
ka saurari abin da zan ce.
17 Maƙiyin gaskiya zai iya yin mulki?
Za ka iya ba mai gaskiya, Maɗaukaki laifi?
18 Ba shi ne ya ce wa sarakuna, ‘Ba ku da amfani ba,’
ya ce wa manya ‘Ku mugaye ne,’
19 wanda ba ya nuna sonkai ga ’ya’yan sarki
kuma ba ya goyon bayan masu arziki a kan matalauta,
gama dukansu shi ya yi su da hannuwansa.
20 Suna mutuwa nan take, a cikin tsakiyar dare;
an girgiza mutanen amma sun wuce;
an taɓa manya amma ba da hannun mutum ba.

21 “Idanunsa suna kan al’amuran mutane;
yana ganin tafiyarsu duka.
22 Babu wuri mai duhu, babu inuwa mai duhu,
inda masu aikata mugunta za su ɓoye.
23 Allah ba ya bukata yă ci gaba da bincike mutane,
har da za su zo gabansa don yă shari’anta su.
24 Ba tare da tambaya ba yana ragargaza masu iko,
yă kuma sa waɗansu a wurinsu.
25 Gama yana sane da abubuwan da suke yi,
yana hamɓarar da su da dare a kuma ragargaza su.
26 Yana ba su horo, don muguntarsu,
inda kowa zai gan su,
27 domin sun juya daga binsa,
kuma ba su kula da hanyoyinsa ba.
28 Sun sa kukan matalauta ya kai wurinsa
yadda ya kai ga jin kukan masu bukata.
29 Amma in ya yi shiru, wa zai ba shi laifi?
In ya ɓoye fuskarsa, wa zai gan shi?
Duk da haka shi yake da iko kan mutum da al’umma duka,
30 yana hana wanda bai san Allah ba yă yi mulki,
ya hana shi sa wa mutane tarko.

31 “A ce mutum ya ce wa Allah, ‘Na yi laifi,
amma ba zan sāke saɓa wa wani ba.
32 Ka koya mini abin da ba zan iya gani ba;
in na yi ba daidai ba, ba zan sāke yi ba.’
33 Ya kamata Allah yă yi maka bisa ga abin da ka ce ne,
sa’ad da ka ƙi ka tuba?
Dole kai ka zaɓa, ba ni ba;
yanzu ka gaya mini abin da ka sani.

34 “Mutane masu ganewa za su ce,
masu hikima waɗanda suka ji ni za su ce mini,
35 ‘Ayuba ya yi magana cikin rashin sani;
maganganunsa na marar hikima ne.’
36 Kash, da za a gwada Ayuba har ƙarshe,
domin yana ba da amsa kamar mugun mutum.
37 Ya ƙara tawaye a kan zunubansa;

ya tafa hannuwansa na reni a cikinmu
ya kuma ƙara yawan maganganunsa ga Allah."

## 35

1 Sai Elihu ya ce,
2 "Ko kana tsammani wannan gaskiya ne?
Kana cewa, 'Ni mai adalci ne a gaban Allah.'
3 Duk da haka kana tambayarsa cewa, 'Wace riba nake da ita,
kuma mene ne zan samu ta wurin ƙin yin zunubi?'

4 "Zan so in ba ka amsa
kai tare da abokanka.
5 Ku ɗaga kai ku dubi sama ku gani;
ku dubi gizagizai a samanku.
6 In kun yi zunubi ta yaya wannan zai shafi Allah?
In zunubanku sun yi yawa, me wannan zai yi masa?
7 In kuna da adalci, me kuka ba shi,
ko kuma me ya karɓa daga hannunku?
8 Muguntarku takan shafi mutum kamar ku ne kaɗai,
adalcinku kuma yakan shafi 'yan adam ne kaɗai.

9 "Mutane suna kuka don yawan zalunci;
suna roƙo don taimako daga hannu mai ƙarfi.
10 Amma ba wanda ya ce, 'Ina Allah wanda ya halicce ni,
mai ba da waƙoƙi cikin dare,
11 wanda ya fi koya mana fiye da dabbobin duniya
ya kuma sa muka fi tsuntsayen cikin iska hikima.'
12 Ba ya amsawa lokacin da mutane suka yi kira don taimako
domin girman kan mugaye.
13 Lalle Allah ba ya sauraron roƙonsu na wofi;
Maɗaukaki ba ya kula da roƙonsu.
14 Ta yaya zai saurara sosai ko zai saurara
lokacin da kake cewa ba ka ganinsa,
cewa ka kawo ƙara a wurinsa
kuma dole ka jira shi.
15 Kuma ka ce, ba ya ba da horo cikin fushinsa
ko kaɗan ba ya kula da mugunta.
16 Saboda haka Ayuba ya buɗe baki yana magana barkatai;
yana ta yawan magana ba tare da sani ba."

## 36

1 Elihu ya ci gaba,
2 "Ka ɗan ƙara haƙuri da ni kaɗan,
zan kuma nuna maka cewa akwai sauran abubuwan da zan faɗa a madadin Allah.
3 Daga nesa na sami sanina;
zan nuna cewa Mahaliccina shi mai gaskiya ne.
4 Abin da zan gaya maka ba ƙarya ba ne;
mai cikakken sani yana tare da kai.

5 "Allah mai iko ne, amma ba ya rena mutane;

shi mai girma ne cikin manufarsa.
6 Ba ya barin mugaye da rai
sai dai yana ba waɗanda ake tsanantawa hakkinsu.
7 Ba ya fasa duban masu adalci;
yana sa su tare da sarakuna
yana ɗaukaka su har abada.
8 Amma in mutane suna daure da sarƙoƙi,
ƙunci kuma ya daure su,
9 yana gaya musu abin da suka yi,
cewa sun yi zunubi da girman kai.
10 Yana sa su saurari gyara yă kuma umarce su
su tuba daga muguntarsu.
11 In sun yi biyayya suka bauta masa,
za su yi rayuwa dukan kwanakinsu cikin wadata
shekarunsu kuma cikin kwanciyar zuciya.
12 Amma in ba su saurara ba,
za su hallaka da takobi
kuma za su mutu ba ilimi.

13 “Waɗanda ba su da Allah a zuciyarsu su ne suke riƙe fushi;
ko sa’ad da ya ba su horo, ba su neman taimakonsa.
14 Suna mutuwa tun suna matasa,
cikin ƙazamar rayuwar karuwanci.
15 Amma yana kuɓutar da masu wahala;
yana magana da su cikin wahalarsu.

16 “Yana so yă rinjaye ka daga haƙoran ƙunci,
zuwa wuri mai sauƙi inda ba matsi
zuwa teburinka cike da abincin da kake so.
17 Amma yanzu an cika ka da hukuncin da ya kamata a yi wa mugaye;
shari’a da kuma gaskiya sun kama ka.
18 Ka yi hankali kada wani yă ruɗe ka da arziki;
kada ka bar toshiya ta sa ka juya.
19 Dukiyarka
ko dukan yawan ƙoƙarinka
sun isa su riƙe ka su hana ka shan ƙunci?
20 Kada ka yi marmari dare yă yi,
don a fitar da mutane daga gidajensu.
21 Ka kula kada ka juya ga mugunta,
abin da ka fi so fiye da wahala.

22 “An ɗaukaka Allah cikin ikonsa.
Wane ne malami kamar sa?
23 Wane ne ya nuna masa hanyar da zai bi,
ko kuma wane ne ya ce masa, ‘Ba ka yi daidai ba?’
24 Ka tuna ka ɗaukaka aikinsa,
waɗanda mutane suka yaba a cikin waƙa.
25 Dukan ’yan adam sun gani;
mutane sun hanga daga nesa.
26 Allah mai girma ne,
ya wuce ganewarmu!
Yawan shekarunsa ba su bincikuwa.

27 “Yana sa ruwa yă zama tururi
yă zubo daga sama.
28 Gizagizai suna zubo da raɓarsu
kuma ruwan sama yana zubowa ’yan adam a wadace.
29 Wane ne zai iya gane yadda ya shimfiɗa gizagizai
yadda yake tsawa daga wurin zamansa?
30 Dubi yadda ya baza walƙiyarsa kewaye da shi,
tana haskaka zurfin teku.
31 Haka yake mulkin al’ummai
yana kuma tanada abinci a wadace.
32 Yana cika hannuwansa da walƙiya
kuma yana ba ta umarni tă fāɗi a inda ya yi nufi.
33 Tsawarsa tana nuna cewa babbar iska da ruwa suna zuwa;
ko shanu sun san da zuwansa.

# 37

1 “Wannan ya sa gabana ya fāɗi,
zuciyata ta yi tsalle.
2 Ka saurara! Ka saurari rurin muryarsa,
tsawar da take fita daga bakinsa.
3 Ya saki walƙiyarsa, a ƙarƙashin dukan sammai
ya kuma aika ta ko’ina a cikin duniya.
4 Bayan wannan sai ƙarar rurinsa ta biyo;
Ya tsawata da muryarsa mai girma.
Sa’ad da ya sāke yin tsawa
ba ya rage wani abu.
5 Muryar Allah tana tsawatawa a hanyoyi masu ban al’ajabi;
yana yin manyan abubuwa waɗanda sun wuce ganewarmu.
6 Yakan ce wa dusar ƙanƙara, ‘Fāɗo a kan duniya,’
ya kuma ce wa ruwa, ‘Zubo da ƙarfi.’
7 Domin dukan mutanen da ya halitta za su san aikinsa,
ya hana kowane mutum yin wahalar aiki.
8 Dabbobi sun ɓoye;
sun zauna cikin kogunansu.
9 Guguwa tana fitowa daga inda take,
sanyi kuma daga iska mai sanyi.
10 Da numfashinsa Allah yana samar da ƙanƙara
sai manyan ruwaye su zama ƙanƙara.
11 Yana cika gizagizai da lema;
yana baza walƙiyarsa ta cikinsu.
12 Bisa ga bishewarsa suke juyawa
a kan fuskar duniya,
suna yin dukan abin da ya
umarce su su yi.
13 Yana aiko da ruwa domin horon mutane,
ko kuma don yă jiƙa duniya yă kuma nuna ƙaunarsa.

14 “Ka saurari wannan Ayuba;
ka tsaya ka dubi abubuwan al’ajabi na Allah.
15 Ko ka san yadda Allah yake iko da gizagizai

ya kuma sa walƙiyarsa ta haskaka?
16 Ko ka san yadda gizagizai suke tsayawa cik a sararin sama,
wadannan abubuwa al'ajabi na mai cikakken sani.
17 Kai mai sa kaya don ka ji ɗumi lokacin da
iska mai sanyi take hurawa,
18 ko za ka iya shimfiɗa sararin sama tare da shi
da ƙarfi kamar madubi?

19 "Gaya mana abin da ya kamata mu ce masa;
ba za mu iya kawo ƙara ba domin duhunmu.
20 Ko za a gaya masa cewa ina so in yi magana?
Ko wani zai nemi a haɗiye shi?
21 Yanzu ba wanda zai iya kallon rana,
yadda take da haske a sararin sama
bayan iska ta share ta.
22 Yana fitowa daga arewa da haske na zinariya,
Allah yana zuwa da ɗaukaka mai ban al'ajabi.
23 Maɗaukaki ya fi ƙarfin ganewarmu,
shi babban mai iko ne, mai gaskiya da babban adalci,
ba ya cutar mutum.
24 Saboda haka, mutane suke girmama shi,
ko bai kula da waɗanda suke gani su masu hikima ba ne?"

## 38

*UBANGIJI ya yi magana*

1 Sa'an nan UBANGIJI ya amsa wa Ayuba. Ya ce,
2 "Wane ne wannan da yake ɓata mini shawarata
da surutan wofi?
3 Ka sha ɗamara kamar namiji;
zan yi maka tambaya,
za ka kuwa amsa mini.

4 "Kana ina lokacin da na aza harsashen duniya?
Gaya mini, in ka sani.
5 Wane ne ya zāna girmanta? Ba shakka ka sani!
Wane ne ya ja layin aunawa a kanta?
6 A kan me aka kafa tushenta,
ko kuma wa ya sa dutsen kan kusurwarta,
7 yayinda taurarin safe suke waƙa tare
dukan mala'iku kuma suka yi sowa don farin ciki.

8 "Wane ne ya rufe teku a bayan ƙofofi,
lokacin da ya burtsatso daga cikin ciki.
9 Lokacin da na yi wa gizagizai riga
na kuma naɗe su a cikin duhu sosai,
10 sa'ad da na yi masa iyaka na
sa masa ƙofofi da wurin kullewa.
11 Sa'ad da na ce ga iyakar inda za ka kai,
ga inda raƙuman ruwanka za su tsaya?

12 "Ko ka taɓa ba safiya umarni

ko kuma ka sa asuba ta fito,
13 don ta kama gefen duniya
ta kakkaɓe mugaye daga cikinta?
14 Kasa ta sāke siffa kamar laka da aka yi wa hatimi;
ta fito a fili kamar riga.
15 An hana mugaye haskensu,
hannun da suka ɗaga an karya shi.

16 "Ko ka taɓa tafiya zuwa maɓulɓulan teku,
ko kuma ka taɓa zuwa cikin zurfin lungun teku?
17 Ko an taɓa nuna maka ƙofar mutuwa?
Ko ka taɓa ganin ƙofar inuwar duhun mutuwa?
18 Ko ka gane fāɗin duniya?
Gaya mini, in ka san wannan duka.

19 "Ina ne hanyar zuwa gidan haske?
Kuma a ina duhu yake zama?
20 Ko za ka iya kai su wurarensu?
Ka san hanyar zuwa wurin da suke zama?
21 Ba shakka ka sani, gama an riga an haife ka a lokacin!
Ka yi shekaru da yawa kana rayuwa.

22 "Ka taɓa shiga rumbunan dusar ƙanƙara
ko ka taɓa ganin rumbunan ƙanƙara
23 waɗanda nake ajiya domin lokacin wahala,
domin kwanakin yaƙi da faɗa?
24 Ina ne hanyar zuwa wurin da ake samun walƙiya,
ko kuma inda daga nan ne ake watsa iskar gabas zuwa ko'ina cikin duniya?
25 Wane ne ya yanka hanyar wucewar ruwa,
da kuma hanyar walƙiyar tsawa
26 don ba da ruwa a ƙasar da ba kowa a wurin
jeji inda ba mai zama ciki
27 don a ƙosar da wurin da ya bushe
a sa ciyawa ta tsiro a can?
28 Ruwan sama yana da mahaifi?
Wa ya zama mahaifin raɓa?
29 Daga cikin wane ne aka haifi ƙanƙara?
Wane ne ya haifi jaura daga sammai
30 lokacin da ruwa ya zama da ƙarfi kamar dutse,
lokacin da saman ruwa ya daskare?

31 "Za ka iya daure kyakkyawar kaza da 'ya'yanta?
Ko za ka iya kunce igiyoyin mafarauci da kare da zomo?
32 Za ka iya tattara taurari bisa ga lokacinsu
ko kuma ka bi da beyar da 'ya'yanta zuwa waje?
33 Ka san dokokin sammai?
Ko za ka iya faɗar dangantakar Allah da duniya?

34 "Za ka iya tsawata wa gizagizai
ka kuma rufe kanka da ambaliyar ruwa?
35 Kai ne kake aika walƙiya da tsawa zuwa inda suke zuwa?

Ko suna zuwa wurinka su ce, ‘Ga mu nan mun zo?’
36 Wane ne yake cika zuciya da hikima
ko kuma yake ba zuciya ganewa?
37 Wane ne yake da hikimar iya ƙirga gizagizai?
Wane ne zai iya karkato bakunan tulunan sammai
38 sa’ad da ƙura ta yi yawa
ta daskare a wuri ɗaya?

39 “Za ka iya farauto wa zakanya nama,
ka kuma kawar wa zakoki yunwarsu.
40 Lokacin da suka kwanta cikin kogunansu,
ko kuma lokacin da suke a wurin ɓuyansu?
41 Wane ne yake ba hankaka abinci
lokacin da ’ya’yansa suke kuka ga Allah,
kuma suna yawo don rashin abinci?

# 39

1 “Ka san lokacin da awakin kan dutse suke haihuwa?
Ko ka taɓa lura da yadda batsiya take haihuwa?
2 Kana ƙirga watanni nawa suke yi kafin su haihu?
Ka san lokacin da suke haihuwa?
3 Suna kwanciya su haifi ’ya’yansu;
naƙudarsu ta ƙare bayan sun haihu.
4 ’Ya’yansu suna girma kuma suna girma cikin ƙarfi a jeji;
sukan tafi ba su dawowa.

5 “Wane ne yake sakin jakin dawa yă bar shi?
Wane ne yake kunce igiyoyinsu?
6 Na sa jeji yă zama gidansa
ƙasar gishiri kuma ta zama wurin zamansa.
7 Yana dariyar hargitsin da yake faruwa a cikin gari;
ba ya jin tsawar mai tuƙa shi.
8 Yana kiwo a kan tuddai don abincinsa
yana neman kowane ɗanyen abu mai ruwan ciyawa.

9 “Ko ɓauna zai yarda yă zauna a wurin sa wa dabbobi abinci?
Zai tsaya a ɗakin dabbobinka da dare?
10 Ko za ka iya daure shi da igiya a kwarin kunya?
Zai yi maka buɗar gonarka?
11 Ko za ka dogara da shi don yawan ƙarfinsa?
Za ka bar masa nauyin aikinka?
12 Ko za ka amince da shi yă kawo maka hatsinka gida
yă tattara shi a masussuka?

13 “Fikafikan jimina suna bugawa cike da farin ciki
amma ba za su gwada kansu da fikafikan da na shamuwa ba.
14 Tana sa ƙwai nata a ƙasa
kuma ta bar su su yi ɗumi a cikin ƙasa,
15 ba tă damu ko za a taka su a fasa su,
ko waɗansu manyan dabbobi za su tattake su.

16 Tana tsananta wa ’ya’yanta kamar ba nata ba
ba tă damu da wahalar da ta sha ba.
17 Gama Allah bai ba ta hikima ba
ko kuma iya fahimta.
18 Duk da haka sa’ad da ta buɗe fikafikanta ta shara da gudu
tana yi wa doki da mai hawansa dariya.

19 “Ko kai ne kake ba doki ƙarfinsa
kai kake rufe wuyansa da geza mai yawa?
20 Ko kai kake sa shi yă yi tsalle kamar fāra,
ba ya jin tsoro sai dai a ji tsoronsa.
21 Yana takawa da ƙarfi
yana jin daɗin ƙarfinsa yana shiga filin yaƙi gabagadi.
22 Yana yi wa tsoro dariya
ba ya jin tsoron kome; ba ya guje wa takobi.
23 Kwari a baka yana lilo a gabansa
kibiya da māshi suna wuce kansa.
24 Yana kartar ƙasa da ƙarfi;
ba ya iya tsayawa tsab sa’ad da ya ji busar ƙaho.
25 Da jin ƙarar ƙaho sai ya ce, ‘Yauwa!’
Ya ji ƙanshin yaƙi daga nesa,
da ihun shugabannin yaƙi.

26 “Ko ta wurin hikimarka ce shirwa take firiya
take kuma baza fikafikanta zuwa kudu?
27 Ko da umarninka ne shaho yake firiya
ya kuma yi sheƙarsa a can sama?
28 Yana zama a kan dutse yă zauna a wurin da dare;
cikin duwatsu ne wurin zamansa.
29 Daga can yake neman abincinsa;
idanunsa suna gani daga nesa.
30 ’Ya’yansa suna shan jini,
inda akwai waɗanda aka kashe nan za a same shi.”

# 40

1 UBANGIJI ya ce wa Ayuba,
2 “Mai neman sa wa wani laifi zai iya ja da Maɗaukaki?
Bari mai tuhumar Allah yă amsa masa.”
3 Sai Ayuba ya amsa wa UBANGIJI,
4 “Ai, ni ba a bakin kome nake ba ne, ta yaya zan iya amsa maka?
Na rufe bakina da hannuna.
5 Na yi magana sau ɗaya amma ba ni da amsa,
sau biyu, amma ba zan ƙara cewa kome ba.”
6 Sa’an nan UBANGIJI ya yi wa Ayuba magana ta cikin guguwa,
7 “Ka tashi tsaye ka tsaya da ƙarfi kamar namiji;
zan yi maka tambaya
kuma za ka amsa mini.

8 “Ko za ka ƙi yarda da shari’ata?
Za ka ba ni laifi don ka nuna kai marar laifi ne?
9 Ko hannunka irin na Allah ne,
kuma ko muryarka za tă iya tsawa kamar ta Allah?

10 Sai ka yi wa kanka ado da ɗaukaka da girma,
ka yafa daraja da muƙami.
11 Ka saki fushinka,
ka dubi dukan wani mai girman kai ka wulaƙanta shi.
12 Ka dubi duk wani mai girman kai ka ƙasƙantar da shi,
ka tattake mugaye a inda ka tsaya.
13 Ka bizne su duka tare
ka rufe fuskokinsu a cikin kabari.
14 Sa'an nan ni kaina zan shaida maka cewa
hannun damanka zai iya cetonka.

15 "Dubi dorina,
wadda na halicce ku tare
kuma ciyawa take ci kamar sa.
16 Ga shi ƙarfinta yana a ƙugunta
ikonta yana cikin tsokar cikinta.
17 Wutsiyarta tana da ƙarfi kamar itacen al'ul;
jijiyoyin cinyoyinta suna haɗe a wuri ɗaya.
18 Kasusuwanta bututun tagulla ne,
haƙarƙarinta kamar sandunan ƙarfe.
19 Tana ta farko cikin ayyukan Allah,
Mahaliccinta kaɗai yake iya tunkarar ta da takobi.
20 Tuddai su suke tanada mata abinci
a inda duk namun jeji suke wasa.
21 Tana kwanciya a ƙarƙashin inuwar itacen lotus
ta ɓuya cikin kyauro da fadama.
22 Inuwa ta rufe ta da ƙaddaji,
itatuwan wardi na rafi, sun kewaye ta.
23 Sa'ad da kogi ya cika yana hauka, ba tă damu ba;
ba abin da zai same ta ko da a gaban bakinta Urdun yake wucewa.
24 Ko akwai wanda zai iya kama ta ba ta kallo,
ko kuma a kama ta da tarko a huda hancinta?

# 41

1 "Ko za ka iya kama dodon ruwa da ƙugiyar kamar kifi
ko kuma ka daure harshenta da igiya?
2 Za ka iya sa igiya a cikin hancinta
ko kuma ka huda muƙamuƙanta da ƙugiya?
3 Za tă ci gaba da roƙonka ka yi mata jinƙai?
Ko za tă yi maka magana a hankali?
4 Za tă yi yarjejjeniya da kai
don ka ɗauke ta tă zama baiwa gare ka dukan kwanakin ranta?
5 Za ka yi wasa da ita kamar yadda za ka yi da tsuntsu?
Ko za ka daure ta da tsirkiya domin bayinka mata?
6 'Yan kasuwa za su saye ta
ko za su raba ta a tsakaninsu?
7 Ko za ka iya huda fatarta da kibiya
ka kuma huda kansa da māsu?
8 In ka ɗora hannunka sau ɗaya a kanta
za ka tuna da yaƙin da ba za ka sāke yi ba!
9 Duk ƙoƙarin kama ta banza ne;

ganin ta kawai abin tsoro ne.
10 Ba wanda ya isa yă tsokane ta.
Wane ne kuma ya isa yă yi tsayayya da ni?
11 Wane ne yake bi na bashi da dole in biya?
Duk abin da yake ƙarƙashin sama nawa ne.

12 "Ba zan daina magana game da gaɓoɓinta ba
ƙarfinta da kuma kyan kamanninta ba.
13 Wa zai iya tuɓe mata mayafinta?
Wa zai iya shiga tsakanin ɓawonta.
14 Wa zai iya buɗe ƙofofin bakinta?
Haƙoranta ma abin tsoro ne?
15 An rufe bayanta da jerin garkuwoyi
aka manne su sosai.
16 Suna kurkusa da juna yadda
da ƙyar iska take iya wucewa tsakani.
17 An haɗa su da juna
sun mannu da juna kuma ba za a iya raba su ba.
18 Numfashinta yana fitar da wuta;
idanunta kamar hasken zuwan safe.
19 Wuta tana fitowa daga bakinta;
tartsatsin wuta suna fitowa,
20 Hayaƙi yana fitowa daga hancinta
kamar daga tukunya mai tafasa a kan wutar itace.
21 Numfashinta yana sa garwashi yă kama wuta,
harshen wuta yana fita daga bakinta.
22 Akwai ƙarfi a cikin wuyanta;
razana tana wucewa a gabanta.
23 Namanta yana da kauri a manne da juna;
naman yana da tauri ba ya matsawa.
24 Kirjinta yana da ƙarfi kamar dutse,
da ƙarfi kamar dutsen niƙa.
25 Sa'ad da ta tashi, manya suna tsorata;
suna ja da baya.
26 Takobi ba ta iya yankanta,
kibiya ko māshi ba sa iya huda ta.
27 Karfe kamar kara ne a wurinta
tagulla kuma kamar ruɓaɓɓen katako ne a wurinta.
28 Māsu ba su sa ta tă gudu;
jifar majajjawa kamar na ciyawa ne gare ta.
29 Kulki a gare ta kamar ciyawa ne,
tana dariyar wucewar māshi.
30 Cikinta yana rufe a ɓawo masu ƙarfi,
tana kabtar ƙasa in tana tafiya.
31 Tana sa zurfin kogi yă tafasa kamar tukunya,
ta kuma sa teku yă zama kamar tukunyar man shafawa.
32 A bayanta ya bar haske
kamar zurfin ruwan da yana kumfa.
33 Ba wani abu kamar ta a duniya,
halitta marar tsoro.
34 Tana rena duk masu girman kai.

Ita take mulki kan duk masu girman kai."

# 42

*Ayuba*

1 Sa'an nan Ayuba ya amsa wa UBANGIJI,
2 "Na san cewa za ka iya yin dukan abubuwa;
ba wanda zai iya ɓata shirinka.
3 Ka yi tambaya, 'Wane ne wannan da ya ƙi karɓar shawarata shi marar ilimi?'
Ba shakka na yi magana game da abubuwan da ban gane ba,
abubuwan ban al'ajabi da sun fi ƙarfin ganewata.

4 "Ka ce, 'Saurara yanzu, zan kuma yi magana
zan tambaye ka,
kuma za ka amsa mini.'
5 Kunnuwana sun ji game da kai
amma yanzu na gan ka.
6 Saboda haka na rena kaina
na kuma tuba cikin ƙura da toka."

*Karshen magana*

7 Bayan UBANGIJI ya gaya wa Ayuba waɗannan abubuwa, ya ce wa Elifaz mutumin
Teman, "Ina fushi da kai da abokanka guda biyu domin ba ku faɗi abin da yake
daidai game da ni ba, kamar yadda bawana Ayuba ya yi. 8 Saboda haka yanzu sai ku
ɗauki bijimai guda bakwai, da raguna bakwai, ku je wurin bawana Ayuba ku miƙa
hadaya ta ƙonawa domin kanku. Bawana Ayuba zai yi muku addu'a zan kuwa karɓi
addu'arsa in bi da ku nisa da wawancinku. Ba ku faɗi abin da yake daidai game da
ni ba yadda bawana Ayuba ya yi ba." 9 Saboda haka Elifaz mutumin Teman, Bildad
mutumin Shuwa da Zofar mutumin Na'ama, suka yi abin da UBANGIJI ya gaya masu;
UBANGIJI kuma ya karɓi addu'ar Ayuba.
10 Bayan Ayuba ya yi wa abokansa addu'a, UBANGIJI ya sa shi ya sāke zama mai
arziki ya ninka abin da yake da shi a dā sau biyu. 11 Dukan 'yan'uwansa maza da
mata da duk waɗanda suka san shi a dā suka zo suka ci abinci tare da shi a cikin
gidansa. Suka ta'azantar da shi suka ƙarfafa shi game da duk wahalar da UBANGIJI
ya auka masa, kowannensu kuma ya ba shi azurfa da zobe na zinariya.
12 UBANGIJI ya albarkaci ƙarshen Ayuba fiye da farkonsa. Yana da tumaki guda
dubu goma sha huɗu, raƙuma guda dubu shida; shanun noma guda dubu da jakuna
guda dubu. 13 Ya kuma haifi 'ya'ya maza bakwai, mata uku. 14 'Yar farko ya kira ta
Yemima, ta biyun Keziya ta ukun Keren-Haffuk. 15 Duk a cikin ƙasar ba a samu
kyawawan mata kamar 'ya'yan Ayuba ba, kuma babansu ya ba su gādo tare ta
'yan'uwansu maza.
16 Bayan wannan Ayuba ya rayu shekara ɗari da arba'in; ya ga 'ya'yansa da
'ya'yansu har tsara ta huɗu. 17 Sa'an nan Ayuba ya rasu da kyakkyawan tsufa.

# Zabura
## LITTAFI NA ƊAYA
## 1

*Zabura 1–41*

1 Mai farin ciki ne mutumin
da ba ya aiki da shawarar mugaye
ko yă yi abin da masu zunubi suke yi
ko yă zauna tare da masu yin ba'a.
2 Amma yana jin daɗin bin dokar UBANGIJI,
kuma yana ta nazarinta dare da rana.
3 Yana kama da itacen da aka shuka kusa da maɓulɓulan ruwa,
wanda yake ba da amfani a daidai lokaci
wanda kuma ganyensa ba sa bushewa.
Duk abin da yake yi, yakan yi nasara.

4 Ba haka yake da mugaye ba!
Su kamar yayi ne
da iska take kwashewa.
5 Saboda haka mugaye ba za su iya tsayawa a shari'a ba,
balle a sami masu zunubi a taron adalai.

6 Gama UBANGIJI yana lura da yadda adalai suke yin abubuwa,
amma ayyukan mugaye za su kai su ga hallaka.

## Zabura 2

1 Me ya sa ƙasashe suke haɗa baki
mutane kuma suke ƙulla shawarwarin banza?
2 Sarakunan duniya sun ɗauki matsayi
masu mulki sun taru gaba ɗaya
suna gāba da UBANGIJI da kuma Shafaffensa.
3 Suna cewa, "Bari mu tsittsinke sarƙoƙinsu,
mu kuma 'yantar da kamammu daga kangin bautar Allah."

4 Mai zama a kursiyi a sama yana dariya;
Ubangiji yana musu ba'a.
5 Sa'an nan ya tsawata musu cikin fushinsa
ya kuma razanar da su cikin hasalarsa, yana cewa,
6 "Na kafa Sarkina a kan kursiyi
a kan Sihiyona, dutsena mai tsarki."
7 Sarki ya yi shelar umarnin UBANGIJI.
UBANGIJI ya ce mini, "Kai Ɗana ne;
yau na zama Mahaifinka.
8 Ka tambaye ni
zan kuwa sa al'ummai su zama gādonka,
iyakokin duniya su zama mallakarka.
9 Za ka yi mulkinsu da sandan ƙarfe;
za ka farfashe su kucu-kucu kamar tukunyar laka."

10 Saboda haka, ku sarakuna, ku yi wayo;

ku shiga hankalinku, ku masu mulkin duniya.
11 Ku bauta wa UBANGIJI da tsoro
ku kuma yi farin ciki kuna rawar jiki.
12 Ku sumbaci Ɗan, don kada yă yi fushi
ku hallaka a abubuwan da kuke yi,
gama fushinsa zai iya kuna farat ɗaya.
Masu farin ciki ne dukan waɗanda suke neman mafaka daga gare shi.

# Zabura 3

Zabura ta Dawuda. Sa'ad da ya gudu daga ɗansa Absalom.
1 Ya UBANGIJI, abokan gābana nawa ne!
Su nawa suke gāba da ni!
2 Da yawa suna magana a kaina suna cewa,
"Allah ba zai cece shi ba."
Sela
*

3 Amma kai ne garkuwa kewaye da ni, ya UBANGIJI;
ka ba ni ɗaukaka ka kuma ɗaga kaina.
4 Ga UBANGIJI na yi kuka mai ƙarfi,
ya kuwa amsa mini daga tudunsa mai tsarki.
Sela

5 Na kwanta na yi barci;
na kuma farka, gama UBANGIJI yana kiyaye ni.
6 Ba zan ji tsoro ko dubu goma
suka ja dāgā gāba da ni a kowane gefe ba.

7 Ka tashi Ya UBANGIJI!
Ka cece ni, ya Allahna!
Ka bugi dukan abokan gābana a muƙamuƙi;
ka kakkarya haƙoran mugaye.

8 Daga wurin UBANGIJI ne ceto kan zo.
Bari albarkanka yă kasance a kan mutanenka.
Sela

# Zabura 4

Don mai bi da kaɗe-kaɗe. Da kayan kiɗi masu tsirkiya. Ta Dawuda.
1 Ka amsa mini sa'ad da na kira gare ka,
Ya Allahna mai adalci.
Ka ba ni sauƙi daga wahalata;
ka ji tausayina ka kuma ji addu'ata.

2 Har yaushe, ya ku mutane za ku mai da ɗaukakata abin kunya?
Har yaushe za ku ƙaunaci ruɗu ku nemi allolin ƙarya?
Sela
3 Ku san cewa UBANGIJI ya keɓe masu tsoron Allah wa kansa;
UBANGIJI zai ji sa'ad da na yi kira gare shi.

---
* **Zabura 3:2** Kalmar da ba a tabbatar da ma'anarta ba, mai bayyana sau da sau a cikin Zabura; mai yiwuwa kalma ce ta kiɗi.

4 Cikin fushinku kada ku yi zunubi;
sa'ad da kuke kan gadajenku,
ku bincike zukatanku ku kuma yi shiru.
Sela
5 Ku miƙa hadayun da suka dace
ku kuma dogara ga UBANGIJI.

6 Yawanci suna cewa, "Wa zai yi mana alheri?"
Bari hasken fuskarka yă haskaka a kanmu, ya UBANGIJI.
7 Ka cika zuciyata da farin ciki
sa'ad da hatsinsu da sabon ruwan inabinsu ya yi yawa.

8 Zan kwanta in kuma yi barci lafiya,
gama kai kaɗai, ya UBANGIJI,
kake sa mazaunina yă kasance lafiya lau.

# Zabura 5

Don mai bi da kaɗe-kaɗe. Don Busa. Ta Dawuda.
1 Ka saurare kalmomina, ya UBANGIJI,
ka ji ajiyar zuciyata.
2 Ka saurare kukata na neman taimako,
Sarkina da Allahna,
gama gare ka nake addu'a.

3 Da safe, ya UBANGIJI, ka ji muryata;
da safe na gabatar da bukatuna a gabanka
in kuma jira da sa zuciya.
4 Kai ba Allahn da yake jin daɗin mugu ba ne;
gama kana gāba da dukan masu aikata mugunta.
5 Masu fariya ba za su iya tsaya
a gabanka ba.
Kana ƙin duk masu aikata abin da ba daidai ba.
6 Kakan hallaka masu yin ƙarya.
Masu kisankai da mutane masu ruɗu
UBANGIJI yana ƙyama.
7 Amma ni, ta wurin jinƙanka mai girma,
zan shiga gidanka;
da bangirma zan durƙusa
ga haikalinka.

8 Ka bi da ni, ya UBANGIJI, cikin adalcinka
saboda abokan gābana,
ka fayyace hanyarka a gabana.
9 Babu ko kalma guda daga bakinsu da za a dogara da ita;
marmarinsu kawai shi ne su hallakar da waɗansu.
Maƙogwaronsu buɗaɗɗen kabari ne;
da harshensu suna faɗin ƙarya.
10 Ka furta su masu laifi, ya Allah!
Bari makircinsu yă zama fāɗuwarsu.
Ka kore su saboda yawan zunubansu,
saboda sun tayar maka.

11 Amma bari dukan waɗanda suke neman mafaka gare ka su yi murna;
bari kullum su yi ta rerawa saboda farin ciki.
Ka buɗe kāriyarka a bisansu,
domin waɗanda suke ƙaunar sunanka su yi farin ciki a cikinka.

12 Gama tabbatacce, ya Ubangiji, kakan albarkaci adalai;
kakan kewaye su da tagomashinka kamar garkuwa.

# Zabura 6

Don mai bi da kaɗe-kaɗe. Da kayan kiɗi masu tsirkiya. Bisa ga *sheminit.** Ta Dawuda.
1 Ya Ubangiji, kada ka tsawata mini cikin fushinka
ko ka hore ni cikin hasalarka.
2 Ka yi mini jinƙai, Ubangiji, gama na suma;
Ya Ubangiji, ka warkar da ni, gama ƙasusuwana suna zafin ciwo.
3 Raina yana cikin wahala.
Har yaushe, ya Ubangiji, har yaushe?

4 Ka juyo, ya Ubangiji, ka cece ni;
ka cece ni saboda madawwamiyar ƙaunarka.
5 Babu wanda yakan tuna da kai sa'ad da ya mutu.
Wa ke yabonka daga kabari?†

6 Na gaji tiƙis daga nishi.

Dukan dare na jiƙe gadona da kuka
na jiƙe kujerata da hawaye.
7 Idanuna sun rasa ƙarfi da baƙin ciki;
sun rasa ƙarfi saboda dukan abokan gābana.

8 Ku tafi daga gare ni, dukanku masu aikata mugunta,
gama Ubangiji ya ji kukata.
9 Ubangiji ya ji kukata saboda jinƙansa;
Ubangiji ya karɓi addu'ata.
10 Dukan abokan gābana za su sha kunya su kuma karaya;
za su juya da kunya nan da nan.

# Zabura 7

Wani *shiggayiyon** ta Dawuda, wanda Ya Rera wa Ubangiji game da Kush mutumin Benyamin.
1 Ya Ubangiji Allahna, na zo neman mafaka a wurinka;
ka cece ni ka kuɓutar da ni daga dukan waɗanda suke bi na,
2 in ba haka ba za su yayyage ni kamar zaki
su ɓarke ni kucu-kucu ba tare da wani da zai cece ni ba.

3 Ya Ubangiji Allahna, in na yi kuskure
aka kuwa sami laifi a hannuwana,
4 in na yi mugunta ga wanda yake zaman lafiya da ni
ko kuwa ba da wani dalilin cuci abokin gābana,
5 to, bari abokin gābana yă bi yă kuma cim mini;

---

* **Zabura 6:** mai yiwuwa wata kalmar kiɗi ce. † **Zabura 6:5** Da Ibraniyanci Sheol * **Zabura 7:** Kan magana, mai yiwuwa wata kalmar kiɗi ce.

bari yă tattake raina a ƙasa
ya sa in kwana a ƙura.

Sela

6 Ka tashi, ya UBANGIJI, cikin fushinka;
ka tashi gāba da fushin abokan gābana.
Ka farka, Allahna, ka umarta adalci.
7 Bari taron mutane su taru kewaye da kai.
Ka yi mulki a bisansu daga bisa;
8 bari UBANGIJI mai shari'ar mutane.
Ka shari'anta ni Ya UBANGIJI, bisa ga adalcina,
bisa ga mutuncina, ya Mafi Ɗaukaka.
9 Ya Allah mai adalci,
wanda yake binciken tunani da zukata,
ka kawo ƙarshen rikicin mugaye
ka kuma sa adalai su zauna lafiya.

10 Garkuwata shi ne Allah Mafi Ɗaukaka,
wanda yake ceton masu tsabtar zuciya.
11 Allah alƙali ne mai adalci,
Allahn da yakan bayyana fushinsa kowace rana.
12 In mutum bai tuba ba,
Allah zai wasa takobinsa;
zai tanƙware yă kuma ɗaura bakansa.
13 Ya shirya makamansa masu dafi;
ya shirya kibiyoyinsa masu wuta.

14 Wanda yake da cikin mugunta
ya kuma ɗauki cikin damuwa yakan haifi ƙarya.
15 Wanda ya haƙa rami
yakan fāɗa cikin ramin da ya haƙa.
16 Damuwar da ya ja yakan sāke nannaɗe a kansa;
fitinarsa takan sauka a kansa.

17 Zan gode wa UBANGIJI saboda adalcinsa
zan kuma rera yabo ga sunan UBANGIJI Mafi Ɗaukaka.

# Zabura 8

Don mai bi da kaɗe-kaɗe. Bisa ga *gittit.** Zabura ta Dawuda.
1 Ya UBANGIJI, shugabanmu,
sunanka da girma take a cikin dukan duniya!

Ka kafa ɗaukakarka
bisa sammai.
2 Daga leɓunan yara da jarirai
ka kafa yabo domin su sa abokan gābanka
da masu ɗaukan fansa su yi shiru.
3 Sa'ad da na dubi sammai,
aikin yatsotsinka,
wata da taurari

* **Zabura 8:** Kan magana, mai yiwuwa wata kalmar kiɗi ce.

waɗanda ka ajiye a wurarensu,
4 wane ne mutum da kake tunawa da shi,
ɗan mutum da kake lura da shi?

5 Ka yi shi ƙasa kaɗan da Allah†
ka yi masa rawani da ɗaukaka da girma.
6 Ka mai da shi mai mulki bisa ayyukan hannuwanka;
ka sa kome a ƙarƙashin ƙafafunsa,
7 dukan shanu da tumaki,
da kuma namun jeji,
8 tsuntsayen sararin sama
da kifin teku,
da dukan abin da yake yawo a ƙarƙashin ruwan teku.

9 Ya Ubangiji, shugabanmu,
sunanka da girma take a cikin dukan duniya!
*

# Zabura 9

Don mai bi da kaɗe-kaɗe. Ga muryar "Mutuwar Ɗa." Zabura ta Dawuda.
1 Zan yabe ka, ya Ubangiji, da dukan zuciyata;
zan faɗa dukan abubuwan banmamakinka.
2 Zan yi murna in kuma yi farin ciki a cikinka;
zan rera yabo ga sunanka, ya Mafi Ɗaukaka.

3 Abokan gābana sun ja da baya;
suka yi tuntuɓe suka hallaka a gabanka.
4 Gama ka tabbata da gaskiyata da kuma abin da nake yi;
ka zauna a kujerarka, kana yin shari'a da adalci.
5 Ka tsawata wa ƙasashe ka kuma hallakar da mugaye;
ka shafe sunansu har abada abadin.
6 Lalaci marar ƙarewa ya cimma abokan gābanmu,
ka tuttumɓuke biranensu;
yadda ma ba aka ƙara tunaninsu.

7 Ubangiji yana mulki har abada;
ya kafa kujerarsa don shari'a.
8 Zai hukunta duniya da adalci;
zai yi mulkin mutane cikin gaskiya.
9 Ubangiji shi ne mafakan waɗanda ake danniya,
mafaka a lokutan wahala.
10 Waɗanda suka san sunanka za su dogara da kai,
gama kai, Ubangiji, ba ka taɓa yashe waɗanda suke nemanka ba.

11 Rera yabai ga Ubangiji, wanda yake zaune a kursiyi a Sihiyona;
yi shela a cikin al'ummai abin da ya aikata.
12 Gama shi da yakan ɗauki fansa a kan mai kisa yakan tuna;
ba ya ƙyale kukan masu wahala.

---

† **Zabura 8:5** Ko kuwa da rayayyun sama * **Zabura 9:** Mai yiwuwa Zabura 9 da 10 tun ainihi waƙa guda ce, ɓangarori mai ƙunshe da layi masu yawa waɗanda suka fara da harufan Ibraniyancin da suke bin juna. A Seftuwajin zabura guda ce.

13 Ya UBANGIJI, dubi yadda abokan gābana suna tsananta mini!
Ka yi jinƙai ka kuma ɗaga ni daga ƙofofin mutuwa,
14 don in furta yabanka
cikin ƙofofin 'Yar Sihiyona
a can kuwa in yi farin ciki cikin cetonka.

15 Al'umma sun fāɗa cikin ramin da suka haƙa wa waɗansu;
aka kama ƙafafunsu a ragar da suka ɓoye.
16 An san UBANGIJI ta wurin gaskiyarsa;
an kama mugaye da aikin hannuwansu.

Haggayiyon.
Sela

†
17 Mugaye za su koma kabari,
dukan al'umman da suka manta da Allah.
18 Amma har abada ba za a manta da mai bukata ba,
ba kuwa sa zuciyar mai wahala zai taɓa hallaka.

19 Ka tashi, ya UBANGIJI, kada ka bar wani yă yi nasara;
bari a hukunta al'ummai a gabanka.
20 Ka buge su da rawar jiki, ya UBANGIJI;
bari al'ummai su sani su mutane ne kurum.

Sela

# * Zabura 10

1 Don me, ya UBANGIJI, kake tsaya can da nesa?
Me ya sa kake ɓoye kanka a lokutan wahala?

2 Cikin fariyarsa mugun mutum yakan cuci marasa ƙarfi,
waɗanda yake kama cikin makircin da ya shirya.
3 Yakan yi taƙama da ƙulle-ƙullen zuciyarsa;
yana albarkaci mai haɗama yana kuma ƙin UBANGIJI.
4 Cikin ɗaga kai mutum ba ya neman Allah;
cikin tunaninsa ba ya ba da wata dama saboda Allah.
5 Hanyoyinsa kullum sukan yi nasara;
yana da girman kai kuma dokokinka suna nesa da shi;
yakan yi wa dukan abokan gābansa duban reni.
6 Yakan ce wa kansa, “Ba abin da zai girgiza ni;
kullum zan yi murna ba zan taɓa shiga wahala ba.”

7 Bakinsa ya cika da zage-zage da ƙarairayi da kuma barazana;
wahala da mugunta suna a ƙarƙashin harshensa.
8 Yakan yi kwanto kusa da ƙauyuka;
daga kwanton yakan kashe marar laifi.
Yana kallon waɗanda za su shiga hannunsa a ɓoye.
9 Yakan yi kwanto a ɓoye kamar zaki.
Yakan yi kwanto don yă kama marasa ƙarfi;
yakan kama marasa ƙarfi yă ja su cikin ragarsa.
10 Yakan ragargaza waɗanda suka shiga hannu, su fāɗi;

---

† **Zabura 9:16** Ko kuwa Tunani; mai yiwuwa salon kiɗi ne. * **Zabura 10:** Mai yiwuwa Zabura 9 da 10 tun ainihi waƙa guda ce, ɓangarori mai ƙunshe da layi masu yawa waɗanda suka fara da harufan Ibraniyancin da suke bin juna. A Seftuwajin zabura guda ce.

sukan fāɗi a ƙarƙashin ƙarfinsa.
11 Yakan ce wa kansa, “Ai, Allah ya manta;
ya rufe fuskarsa ba ya gani.”

12 Ka tashi, UBANGIJI! Ka hukunta miyagu, ya Allah.
Kada ka manta da marasa ƙarfi.
13 Don me mugun mutum zai ƙi Allah?
Don me yakan ce wa kansa,
“Allah ba zai nemi hakki daga gare ni ba”?
14 Amma kai, ya Allah, kana gani wahala da baƙin ciki;
kana lura da yadda suke ɗaukansu a hannu.
Marar taimako kan danƙa kansa gare ka;
kai ne mai taimakon marayu
15 Ka karye hannun mugaye da kuma mugun mutum;
ka nemi hakki daga gare shi saboda muguntar
da ba za a gane ba.

16 UBANGIJI Sarkin har abada abadin ne;
al’ummai za su hallaka daga ƙasarsa.
17 Kakan ji, ya UBANGIJI sha’awar mai shan wahala;
kakan ƙarfafa su, ka kuma saurari kukansu,
18 kana kāre marayu da waɗanda aka danne,
domin mutum, wanda yake na duniya
kada ƙara haddasa wata razana.

# Zabura 11

Don mai bi da kaɗe-kaɗe. Don busa. Ta Dawuda.
1 A wurin UBANGIJI ne nake samun mafaka.
Yaya za ku ce mini,
“Ka yi firiya kamar tsuntsu zuwa duwatsu.
2 Gama duba, mugaye sun tanƙware bakkunansu;
sun kuma ɗana kibiyoyinsu
don su harbi mutanen kirki a zuciya
daga cikin duhu.
3 Sa’ad da aka tumɓuke tushe,
me adali zai iya yi?”

4 UBANGIJI yana cikin haikalinsa mai tsarki;
UBANGIJI yana a kursiyinsa a sama.
Yana kallon ’ya’yan mutane;
idanunsa suna bincike su.
5 UBANGIJI yana bincike adalai,
amma ransa yana ƙi mugaye
da masu son rikici.
6 A kan mugaye zai zuba
garwashin wuta mai zafi da kuma kibiritu;
iska mai zafi zai zama rabonsu.

7 Gama UBANGIJI mai adalci ne,
yana ƙaunar gaskiya
masu adalci za su ga fuskarsa.

# Zabura 12

Don mai bi da kaɗe-kaɗe. Da kayan kiɗi. Bisa ga *sheminit.** Zabura ta Dawuda.

1 Ka taimaka, UBANGIJI, gama masu tsoron Allah ba sa nan kuma;
masu aminci sun ɓace daga cikin mutane.
2 Kowa yana yi wa maƙwabcinsa ƙarya;
zaƙin bakinsu maganar ƙarya ce
suna cike da ruɗu a zukatansu.

3 Bari UBANGIJI yǎ yanke dukan zaƙin bakinsu
da kuma kowane harshe mai fariya,
4 masu cewa,
“Da harsunanmu za mu yi nasara;
leɓunanmu za su kāre mu, wane ne maigidanmu?”

5 “Saboda danniyar marasa ƙarfi da kuma nishin masu bukata,
zan tashi yanzu,” in ji UBANGIJI.
“Zan kāre su daga masu yin musu sharri.”
6 Kalmomin UBANGIJI kuwa ba su da kuskure,
kamar azurfan da aka tace cikin matoyan yumɓu,
aka tsabtacce sau bakwai.

7 Ya UBANGIJI, za ka kiyaye mu lafiya
ka tsare mu daga irin mutanen nan har abada.
8 Mugaye suna yawo a sake
sa’ad da ake girmama abin da ba shi da kyau a cikin mutane.

# Zabura 13

Don mai bi da kaɗe-kaɗe. Zabura ta Dawuda.

1 Har yaushe, ya UBANGIJI? Za ka manta da ni har abada ne?
Har yaushe za ka ɓoye fuskarka daga gare ni?
2 Har yaushe zan yi kokawa da tunanina
kuma kowace rana in kasance da damuwa a zuciyata?
Har yaushe abokin gābana zai yi nasara a kaina?

3 Ka dube ni ka amsa mini, ya UBANGIJI Allahna.
Ka ba da haske ga fuskata, ko in yi barci cikin mutuwa;
4 abokin gābana zai ce, “Na sha ƙarfinsa,”
kuma abokan gābana za su yi murna sa’ad da na fāɗi.

5 Amma na dogara a kan ƙaunarka marar ƙarewa;
zuciyata tana farin ciki a cikin cetonka.
6 Zan rera ga UBANGIJI
gama ya yi mini alheri.

# Zabura 14

Don mai bi da kaɗe-kaɗe. Ta Dawuda.

1 Wawaye sukan ce a ransu,
“Ba Allah.”
Sun lalace, ayyukansu kuwa mugaye ne;
babu wani da yake yi abu mai kyau.

---

* **Zabura 12:** Kan magana, mai yiwuwa wata kalmar kiɗi ce.

2 UBANGIJI ya duba daga sama
a kan ʼyan adam
don yă ga ko akwai wani da ya gane,
wani wanda yake neman Allah.
3 Duka sun kauce, duka gaba ɗaya sun zama lalatattu;
babu ɗaya wanda yake yin abu mai kyau,
ba ko ɗaya.

4 Masu aikata mugunta za su taɓa koyo.

Suna cin mutane yadda mutane ke cin gurasa
kuma waɗanda ba sa kira bisa UBANGIJI?
5 Ga su, tsoro ya sha kansu,
gama Allah yana cikin ƙungiyar adalai.
6 Ku masu mugunta kuna sa ƙoƙarin matalauta yă zama banza,
amma UBANGIJI ne mafakansu.

7 Kash, da ceton Israʼila zai fito daga Sihiyona mana!
Saʼad da UBANGIJI zai maido da saʼar mutanensa,
bari Yaƙub yă yi farin ciki Israʼila kuma yă yi murna!

# Zabura 15

Zabura ta Dawuda.
1 UBANGIJI, wa zai zauna cikin wuri mai tsarkinka?
Wa zai zauna a kan tudunka mai tsarki?

2 Sai wanda ba shi da laifi
kuma yana yin abin da yake daidai,
wanda yake faɗin gaskiya daga zuciyarsa
3 ba ya kuwa ɓata sunan wani da harshensa,
wanda ba ya yi wa maƙwabcinsa mugunta
ba ya kuwa baza jita-jita a kan ɗanʼuwansa,
4 wanda yake ƙin mugun mutum
amma yakan girmama masu tsoron UBANGIJI,
yakan cika alkawarinsa
ko da ma ya zafe shi,
5 wanda yake ba da rance ba tare da ruwa ba
kuma ba ya karɓan cin hanci don yă kā da marar laifi.

Shi wanda yake yin waɗannan abubuwa
ba zai taɓa jijjiguwa ba.

# Zabura 16

*Miktam* ne* na Dawuda.
1 Ka kiyaye ni, ya Allah,
gama a cikinka nake samun mafaka.

2 Na ce wa UBANGIJI, "Kai ne shugabana;
in ba tare da kai ba, ba ni da wani abu mai kyau."
3 Game da tsarkakan da suke cikin ƙasar kuwa,

* **Zabura 16:** Kan magana, mai yiwuwa wata kalma ta kiɗa ce.

su ne masu ɗaukakar da dukan farin cikina ya dangana.
4 Baƙin ciki zai ƙaru wa waɗanda suke bin waɗansu alloli.
Ba zan zuba musu hadayarsu ta jini ba
ko in ambaci sunayensu da bakina.

5 UBANGIJI, ka ba ni rabona da kwaf ɗin na;
ka kiyaye rabona,
6 Iyakoki sun fāɗo mini a wurare masu daɗi;
tabbatacce ina da gādo mai bansha'awa.
7 Zan yabi UBANGIJI, wanda yake ba ni shawara;
ko da dare ma zuciyata kan koya mini.
8 Kullum nakan sa UBANGIJI a gabana.
Gama yana a hannun damana, ba zan jijjigu ba.

9 Saboda haka zuciyata tana murna harshena kuma yana farin ciki;
jikina kuma zai zauna lafiya,
10 domin ba za ka yashe ni a kabari ba,
ba kuwa za ka bar Mai Tsarkinka yă ruɓa ba.
11 Ka sanar da ni hanyar rai;
za ka cika ni da farin ciki a gabanka,
da madawwamin jin daɗi a hannun damarka.

# Zabura 17

Addu'a ce ta Dawuda.
1 Ka ji, ya UBANGIJI, roƙona na adalci;
ka saurari kukata.
Ka kasa kunne ga addu'ata,
ba ta fitowa daga leɓuna masu ƙarya.
2 Bari fiffitawata tă zo daga gare ka;
bari idanunka su ga abin da yake daidai.

3 Ko ka duba zuciyata,
ka kuma bincike ni da dare,
ko ka gwada ni, ba za ka sami kome ba;
na yanke shawara cewa bakina ba zai yi zunubi ba.
4 Game da ayyukan mutane kuwa,
ta wurin maganar leɓunanka na kiyaye kaina
daga hanyoyin tashin hankali.
5 Sawuna sun kama hanyoyinka
ƙafafu kuwa ba za su yi santsi ba.

6 Na kira gare ka, ya Allah, gama za ka amsa mini;
ka kasa kunne ka kuma ji addu'ata.
7 Ka nuna mini girmar ƙaunarka mai banmamaki,
kai da kake ceton waɗanda suke neman mafaka daga abokan gābansu
da hannunka na dama.
8 Ka kiyaye ni yadda ake kiyaye ido;
ka ɓoye ni cikin inuwar fikafikanka
9 daga mugaye waɗanda suke kai mini hari,
daga abokan gāba masu mutuwa waɗanda suka kewaye ni.

10 Sun rufe zukatansu marar tausayi,
da bakunansu suna magana da fariya.
11 Sun sa mini ido, yanzu sun kewaye ni,
a shirye suke, su jefa ni a ƙasa.
12 Suna kama da zaki mai yunwan abinci,
kamar babban zaki mai fako a maɓuya.

13 Ka tashi, ya UBANGIJI, ka yi arangama da su, ka durƙusar da su;
ka cece ni daga mugaye ta wurin takobinka.
14 Ya UBANGIJI, da hannunka ka cece ni daga irin mutanen nan,
daga mutanen duniyan nan waɗanda ladarsu yana a wannan rayuwa ne.
Kakan cika yunwan waɗanda kake so;
'ya'yansu suna da isashe
suna kuma ajiyar wadata wa 'ya'yansu.

15 Amma ni, cikin adalci zan ga fuskarka;
sa'ad da na farka, zan gamsu da ganin kamanninka.

# Zabura 18

Don mai bi da kaɗe-kaɗe. Ta Dawuda bawan UBANGIJI. Ya rera ta ga UBANGIJI kalmomin wannan waƙa sa'ad da UBANGIJI ya cece shi daga hannun dukan abokan gābansa da kuma daga hannun Shawulu, ya ce,
1 Ina ƙaunarka, ya UBANGIJI, ƙarfina.

2 UBANGIJI shi ne dutsena, kagarata da kuma mai cetona;
Allahna shi ne dutsena, a gare shi nake neman mafaka.
Shi ne garkuwata da ƙahon cetona, mafakata.

3 Na kira ga UBANGIJI, wanda ya cancanci yabo,
na kuwa kuɓuta daga abokan gābana.
4 Igiyoyin mutuwa sun shaƙe ni;
rigyawan hallaka sun sha kaina.
5 Igiyoyin mutuwa sun nannaɗe kewaye da ni;
tarkon mutuwa ya yi mini arangama.

6 Cikin wahalata na yi kira ga UBANGIJI;
Na yi kuka ga Allahna don taimako.
A Haikalinsa ya ji muryata,
Kukana na neman taimako ya kai kunnensa.
7 Kasa ta yi rawa ta kuma girgiza,
tussan duwatsu sun girgiza;
sun yi rawa domin ya yi fushi.
8 Hayaƙi ya tashi daga kafan hancinsa;
wuta mai ci daga bakinsa,
garwashi wuta mai ci daga bakinsa.
9 Ya buɗe sammai ya sauko;
baƙaƙen gizagizai suna a ƙarƙashin ƙafafunsa.
10 Ya hau kerubobi ya kuma yi firiya;
ya yi shawagi a fikafikan iska.
11 Ya mai da duhu abin rufuwarsa, rumfa kewaye da shi,

bakaken gizagizan ruwan sama na sarari,
12 daga cikin hasken kasancewarsa gizagizai suka yi gaba,
da kankara da kuma walkiya.
13 UBANGIJI ya yi tsawa daga sama;
muryar Mafi Ɗaukaka ya yi kāra.
14 Ya harba kibiyoyinsa ya kuma watsar da abokan gāba,
walkiya mai girma ya fafare su.
15 Kwarin teku sun bayyana
tussan duniya sun bayyana a fili
sa'ad da ka tsawata, ya UBANGIJI,
sa'ad da ka numfasa daga hancinka.

16 Ya mika hannunsa daga sama ya kama ni;
ya ja ni daga zurfin ruwaye.
17 Ya cece ni daga abokin gābana mai karfi,
daga abokan gābana, waɗanda suka fi karfina.
18 Sun yi arangama da ni a ranar masifa,
amma UBANGIJI ya zama mai taimakona.
19 Ya fitar da ni zuwa wuri mai sarari;
ya kuɓutar da ni, gama yana jin daɗina.

20 UBANGIJI ya yi haka da ni bisa ga adalcina;
bisa ga tsabtar hannuwana ya ba ni lada.
21 Gama na kiyaye hanyoyin UBANGIJI;
ban yi mugunta ta wurin juyewa daga Allahna ba.
22 Dukan dokokinsa suna a gābana;
ban juye daga ka'idodinsa ba.
23 Na kasance marar laifi a gabansa
na kuma kiyaye kaina daga zunubi.
24 UBANGIJI ya ba ni lada bisa ga adalcina,
bisa ga tsabtan hannuwana a gabansa.

25 Ga mai aminci ka nuna kanka mai aminci,
ga marar laifi ka nuna kanka marar laifi,
26 ga mai tsabta ka nuna kanka mai tsabta,
amma ga karkatacce, ka nuna kanka mai wayo.
27 Kakan cece mai saukinkai
amma kakan kaskantar da masu girman kai.
28 Kai Ya UBANGIJI, ka sa fitilata ta yi ta ci;
Allahna ya mai da duhu ya zama haske.
29 Da taimakonka zan iya fāɗa wa runduna;
tare da Allahna zan iya rinjayi katanga.

30 Game da Allah kuwa, hanyarsa cikakkiya ce;
maganar UBANGIJI marar kuskure ne.
Shi garkuwa ne ga dukan waɗanda suke neman mafaka a gare shi.
31 Gama wane ne Allah in ba UBANGIJI ba?
Wane ne kuwa Dutse in ba Allahnmu ba?
32 Allah ne ya karfafa ni da karfi
ya kuma sa hanyarta ta zama cikakkiya.
33 Ya sa kafafuna kamar kafafun barewa;

ya sa na iya tsaya a kan ƙwanƙoli.
34 Ya horar da hannuwana don yaƙi;
hannuwana za su iya tanƙware bakan tagulla.
35 Ka ba ni garkuwar nasara,
kuma hannunka na dama yana riƙe ni;
ya sunkuya don ka mai da ni mai girma.
36 Ka fadada hanyar da yake a ƙarƙashina,
don kada ɗiɗɗigena yǎ juya.

37 Na bi abokan gābana na kuma cim musu;
ban juya ba sai da na hallaka su.
38 Na ragargaza su har ba za su iya tashi ba;
sun fāɗi a ƙarƙashin ƙafafuna.
39 Ka ƙarfafa ni da ƙarfi saboda yaƙi;
ka sa abokan gābana suka rusuna mini.
40 Ka sa abokan gābana suka juya suka gudu,
na kuma hallaka abokan gābana.
41 Sun nemi taimako, amma ba su sami wanda zai cece su ba,
ga Ubangiji, amma bai amsa ba.
42 Na murƙushe su kamar ƙura mai laushi da iska ke kwashewa;
na zubar da su kamar laka a rituna.
43 Ka cece ni daga harin mutane;
ka mai da ni kan al'ummai.
Mutanen da ban sani ba sun zama bayina,
44 da zarar sun ji ni, sukan yi mini biyayya;
baƙi suna rusuna a gabana.
45 Duk sukan karai;
suna zuwa da rawan jiki daga mafakansu.

46 Ubangiji mai rai ne! Yabo ya tabbata ga Dutsena!
Girma ya tabbata ga Allah Mai cetona!
47 Shi ne Allah mai sāka mini,
wanda yake sa al'ummai a ƙarƙashina,
48 wanda yakan cece ni daga abokan gābana.
Ana girmama ka bisa abokan gābana;
daga masu tā-da-na-zaune-tsaye ka kuɓutar da ni.
49 Saboda haka zan yabe ka a cikin al'ummai, ya Ubangiji;
zan rera yabai ga sunanka.

50 Yakan ba sarkinsa nasarori;
yakan nuna alheri marar ƙarewa ga shafaffensa,
ga Dawuda da zuriyarsa har abada.

# Zabura 19

Don mai bi da kaɗe-kaɗe. Zabura ta Dawuda.
1 Sammai suna shelar ɗaukakar Allah;
sararin sama suna furta aikin hannuwansa.
2 Kowace rana tana yin jawabi;
kowane dare yana nuna sani.
3 Ba magana, ba kalmar da aka hurta,
ba wani amon da aka ji daga gare su.
4 Duk da haka muryarsu tana kaiwa ga dukan duniya,

kalmominsu zuwa iyakokin duniya.
A sammai Allah ya kafa tenti domin rana,
5 wanda yake kamar ango mai fitowa daga rumfarsa,
kamar gwani ɗan wasan da yake farin ciki yă yi tsere.
6 Takan taso daga ƙarshen sammai
ta kewaye zuwa wancan;
babu abin da yake ɓuya wa zafinta.

7 Dokar UBANGIJI cikakkiya ce,
takan wartsakar da rai.
Farillan UBANGIJI abin dogara ne,
suna mai da hikima da sauƙi.
8 Ka'idodin UBANGIJI daidai ne,
suna ba da farin ciki ga zuciya.
Umarnan UBANGIJI haske ne
suna ba da haske ga idanu.
9 Tsoron UBANGIJI yakan kawo tsabtar zuciya,
zai kasance har abada.
Farillan UBANGIJI tabbatattu ne,
kuma gaba ɗaya masu adalci ne.

10 Sun fi zinariya daraja,
fiye da zalla zinariya nesa;
sun fi zuma zaƙi
fiye da zuma daga kaki.
11 Ta wurinsu ana gargaɗe bawanka;
a kiyaye su akwai lada mai girma.
12 Wane ne zai iya rabe kurakuransa?
Ya gafarta ɓoyayyun laifofinsa.
13 Ka kiyaye bawanka daga zunubin ganganci;
kada ka bari su yi mulki a kaina.
Ta haka zan zama marar laifi;
marar laifi na babban tawaye.

14 Bari kalmomin bakina da tunanin zuciyata
su zama abin gamsuwa a gabanka,
Ya UBANGIJI, Dutsena da Mai fansata.

# Zabura 20

Don mai bi da kaɗe-kaɗe. Zabura ta Dawuda.
1 UBANGIJI ya amsa maka sa'ad da ka yi kira cikin wahala;
bari sunan Allah na Yaƙub yă kiyaye ka.
2 Bari yă aiko maka da taimako daga wuri mai tsarki
yă kuma ba ka gudummawa daga Sihiyona.
3 Bari yă tuna da dukan sadakokinka
yă kuma karɓi hadayunka na ƙonawa.
Sela

4 Bari yă biya maka bukatan ranka
yă kuma sa dukan shirye-shiryenka su yi nasara.
5 Za mu yi sowa ta farin ciki sa'ad da ka yi nasara
mu kuma ɗaga tutotinmu a cikin sunan Allahnmu.

Bari UBANGIJI yǎ biya maka dukan bukatunka.

6 Yanzu na san cewa,
UBANGIJI yakan cece shafaffensa.
Yakan amsa masa daga samansa mai tsarki
da ikon ceto na hannun damansa.
7 Waɗansu sun dogara a kekunan yaƙi waɗansu kuma a dawakai,
amma mu, mun dogara a cikin sunan UBANGIJI Allahnmu.
8 Za a durƙusar da su, su kuma fāɗi,
amma mu za mu tashi mu tsaya daram.
9 Ya UBANGIJI, ka ba da nasara ga sarki!
Ka amsa mana sa'ad da muka yi kira!

# Zabura 21

Don mai bi da kaɗe-kaɗe. Zabura ta Dawuda.
1 Ya UBANGIJI, sarki yana farin ciki cikin ƙarfinka.
Yana farin cikinsa ƙwarai cikin nasarorin da ka ba shi!

2 Ka biya masa bukatar zuciyarsa
ba ka kuwa hana masa roƙon da ya yi da leɓunansa ba.
Sela
3 Ka marabce shi da yalwar albarka
ka kuma sa masa rawanin zallan zinariya a kansa.
4 Ya nemi ka ba shi rai, ka kuwa ba shi,
tsawo kwanaki, har abada abadin
5 Ta wurin nasarorin da ka ba shi, ɗaukakarsa mai girma ce;
ka mayar masa ɗaukaka da kuma suna.
6 Tabbatacce ka ba shi madawwamiyar albarka
ka kuma sa shi murna da farin cikin kasancewarka.
7 Gama sarki ya dogara gare ka UBANGIJI
ta wurin ƙauna marar ƙarewa ta Mafi Ɗaukaka
ba zai jijjigu ba.

8 Hannunka zai kakkama dukan abokan gābanka;
hannunka na dama zai kakkama masu ƙinka.
9 A lokacin bayyanarka
za ka sa su zama kamar wutar matoya.
Cikin fushinsa UBANGIJI zai haɗiye su,
kuma wutarsa za tǎ cinye su.
10 Za ka hallaka 'ya'yansu daga duniya,
zuriyarsu kuma daga 'yan adam.
11 Ko da yake suna shirya maka mugunta
suna kuma ƙirƙiro mugayen dabaru, ba za su yi nasara ba;
12 gama za ka sa su juye bayansu
sa'ad da ka auna su da bakan da ka ja.

13 Ka sami ɗaukaka, ya UBANGIJI cikin ƙarfinka;
za mu rera mu kuma yabi ikonka.

# Zabura 22

Don mai bi da kaɗe-kaɗe. Da salon "Matar Zomon Safiya." Zabura ta Dawuda.
1 Ya Allahna, ya Allahna, don me ka yashe ni?

Me ya sa ka yi nisa da cetona,
ka yi nesa daga kalmomin nishina?
2 Ya Allahna, na yi kuka da rana, amma ba ka amsa ba,
da dare kuma ban yi shiru ba.

3 Duk da haka kana a kursiyi a matsayin Mai Tsarkin nan;
kai ne yabon Isra'ila.
4 A gare ka ne kakanninmu suka sa bege;
sun dogara ka kuwa cece su.
5 Sun yi kuka gare ka suka kuma sami ceto;
a gare ka suka dogara kuma ba su sha kunya ba.

6 Amma ni dai tsutsa ne ba mutum ba,
wanda mutane suke yi wa ba'a suka kuma rena shi.
7 Duk wanda ya gan ni yakan yi mini ba'a;
suna yin mini ashar, suna kaɗa kansu suna cewa,
8 "Ya dogara ga UBANGIJI;
bari UBANGIJI yă cece shi.
Bari yă cece shi,
da yake yana jin daɗinsa."

9 Duk da haka ka fitar da ni daga ciki;
ka sa na dogara gare ka, ko ma a ƙirjin mahaifiyata.
10 Daga haihuwa an jefa ni a kanka;
daga cikin mahaifiyata kai ne Allahna.

11 Kada ka yi nesa da ni,
gama wahala na kusa
kuma babu wani da zai taimaka.

12 Bijimai masu yawa sun kewaye ni;
bijimai masu ƙarfi na Bashan sun sa ni a tsaka.
13 Zakoki masu ruri suna yayyage abin da suka kama
sun buɗe bakunansu a kaina.
14 An zubar da ni kamar ruwa,
kuma dukan ƙasusuwana sun fiffito daga mahaɗai.
Zuciyata ta zama kaki;
ta narke a cikina.
15 Karfina ya bushe kamar kasko,
harshena kuma ya manne wa dasashina na sama;
ka kwantar da ni a ƙurar mutuwa.

16 Karnuka sun kewaye ni;
ƙungiyar mugaye sun sa ni a tsaka,
sun soki hannuwana da ƙafafuna.
17 Zan iya ƙirga ƙasusuwana;
mutane suna farin ciki a kaina.
18 Sun raba rigunana a tsakaninsu
suka kuma jefa ƙuri'a a kan rigunana.

19 Amma kai, ya UBANGIJI, kada ka yi nisa;
Ya Karfina zo da sauri don ka taimake ni.

20 Ka ceci raina daga takobi,
raina mai daraja daga ikon karnuka.
21 Ka cece ni daga bakin zakoki;
ka cece ni daga ƙahonin ɓauna.

22 Zan furta sunanka ga ’yan’uwana;
cikin taron masu sujada zan yabe ka.
23 Ku da kuke tsoron UBANGIJI, ku yabe shi!
Dukanku zuriyar Yaƙub, ku girmama shi!
Ku girmama shi, dukanku zuriyar Isra’ila!
24 Gama bai rena ko yă ƙyale
wahalar masu shan wuya ba;
bai ɓoye fuskarsa daga gare shi ba
amma ya saurari kukansa na neman taimako.

25 Daga gare ka yabona yake zuwa cikin babban taro;
a gaban waɗanda suke tsoronka zan cika alkawarina.
26 Matalauta za su ci su ƙoshi;
su da suke neman UBANGIJI za su yabe shi,
bari zukatanku su rayu har abada!

27 Dukan iyakokin duniya
za su tuna su kuma juya ga UBANGIJI,
kuma dukan iyalan al’ummai
za su rusuna a gabansa,
28 gama mulki na UBANGIJI ne
kuma yana mulki a bisa al’ummai.

29 Dukan attajiran duniya za su yi biki su kuma yi sujada;
dukan waɗanda suka gangara zuwa ƙura za su durƙusa a gabansa,
waɗanda ba za su iya bar kansu da rai ba.
30 Zuriya masu zuwa za su yi masa hidima;
za a faɗa wa zuriya na nan gaba game da Ubangiji.
31 Za su yi shelar adalcinsa
ga mutanen da ba a riga an haifa ba,
gama ya aikata shi.

# Zabura 23

Zabura ta Dawuda.
1 UBANGIJI ne yake kiwona, ba zan rasa kome ba,
2 Yakan sa in kwanta a makiyaya mai ɗanyar ciyawa,
yakan bi da ni kusa da ruwaye marar hayaniya,
3 yakan maido da raina.
Yakan bi da ni a hanyoyin adalci
saboda sunansa.
4 Ko da na yi tafiya
ta kwari na inuwar mutuwa,*
ba zan ji tsoron mugu ba,
gama kana tare da ni;
bulalarka na dūka da kuma sandanka na tafiya,

* **Zabura 23:4** Ko kuwa ta kwarin mafi duhu duka

za su yi mini ta'aziyya.

5 Ka shirya mini tebur
a gaban abokan gābana.
Ka shafe kaina da mai;
kwaf nawa ya cika har yana zuba.
6 Tabbatacce alheri da ƙauna za su bi
dukan kwanakin raina,
zan kuwa zauna a gidan UBANGIJI
har abada.

# Zabura 24

Zabura ta Dawuda.
1 Duniya ta UBANGIJI ce da kome da yake cikinta,
duniya, da dukan waɗanda suke zama a cikinta;
2 gama ya gina ta a kan tekuna
ya kafa ta a kan ruwaye.

3 Wa zai iya hawan tudun UBANGIJI?
Wa zai iya tsaya a wurinsa mai tsarki?
4 Sai wanda yake da hannu mai tsabta da kuma tsabtar zuciya,
wanda ba ya ba da ransa ga bautar gunki
ko ya rantse bisa abin da yake ƙarya.

5 Zai sami albarka daga UBANGIJI
da fiffitawa daga Allah Mai cetonsa.
6 Irin tsaran waɗanda suke nemansa ke nan,
waɗanda suke neman fuskarka, ya Allah na Yaƙub.

Sela

7 Ku ɗaga kawunanku, ya ku ƙofofi;
ku ɗagu, ku daɗaɗɗun ƙofofi,
don Sarkin ɗaukaka yǎ shiga.
8 Wane ne wannan Sarkin ɗaukaka?
UBANGIJI ne mai ƙarfi mai iko,
UBANGIJI mai girma a yaƙi.
9 Ku ɗaga kawunanku, ya ku ƙofofi;
ku ɗagu, ku daɗaɗɗun ƙofofi,
don Sarkin ɗaukaka yǎ shiga.
10 Wane ne shi, wannan Sarkin ɗaukaka?
UBANGIJI Maɗaukaki,
shi ne Sarkin ɗaukaka.

Sela

# * Zabura 25

Ta Dawuda.
1 A gare ka Ya UBANGIJI,
na miƙa raina.

2 A gare ka na dogara, ya Allahna.
Kada ka bari in sha kunya,

* **Zabura 25:** Wannan zabura waƙa ce, mai ayoyin da suke da harufan Ibraniyanci bi da bi.

ko ka bar abokan gābana su yi nasara a kaina.
3 Ba wanda yake sa bege a gare ka
da zai taɓa shan kunya,
amma za su sha kunya
su da suke tayarwa babu dalili.

4 Ka nuna mini hanyoyinka, ya UBANGIJI,
ka koya mini hanyoyinka;
5 ka bi da ni cikin gaskiyarka ka kuma koya mini,
gama kai ne Allah Mai cetona,
kuma begena yana a kanka dukan yini.
6 Ka tuna, ya UBANGIJI da jinƙai da kuma ƙaunarka mai girma,
gama suna nan tun dā.
7 Kada ka tuna da zunuban ƙuruciyata
da kuma hanyoyin tawayena;
bisa ga ƙaunarka ka tuna da ni,
gama kai nagari ne, ya UBANGIJI.

8 UBANGIJI nagari da mai adalci ne;
saboda haka yakan koyar da masu zunubi a hanyoyinsa.
9 Yakan bi da masu tawali'u cikin abin da yake daidai
ya kuma koyar da su hanyoyinsa.
10 Dukan hanyoyin UBANGIJI ƙaunatattu ne da kuma aminci
ga waɗanda suke kiyaye abin da alkawari ya bukaci.
11 Saboda sunanka, ya UBANGIJI,
ka gafarta laifina, ko da yake mai girma ne.

12 To wane ne mai tsoron UBANGIJI?
Zai koyar da shi a hanyar da ya zaɓa masa.
13 Zai ci kwanakinsa a wadace,
kuma zuriyarsa za su gāji ƙasar.
14 UBANGIJI yakan amince da waɗanda suke tsoronsa;
yakan sa su san alkawarinsa.
15 Idanuna kullum suna a kan UBANGIJI,
gama shi ne kaɗai zai kuɓutar da ƙafafuna daga tarko.

16 Ka juye wurina ka kuma yi mini jinƙai,
gama na kaɗaice ina kuma wahala.
17 Damuwoyin zuciyata sun ninka;
ka 'yantar da ni daga wahalata.
18 Ka dubi wahalata da kuma azabata
ka ɗauke mini dukan zunubaina.
19 Dubi yadda abokan gābana sun ƙaru
da kuma yadda suka ƙara ƙina!

20 Ka tsare raina ka kuma kuɓutar da ni;
kada ka bari in sha kunya,
gama na nemi mafaka daga gare ka.
21 Bari mutunci da adalci su tsare ni,
domin begena yana a kanka.

22 Ka fanshi Isra'ila, ya Allah,
daga dukan wahalarsu!

# Zabura 26

Ta Dawuda.
1 Ka nuna rashin laifina, ya UBANGIJI,
gama na yi rayuwa marar zargi;
Na dogara ga UBANGIJI
ba tare da kaucewa ba.
2 Ka jarraba ni, ya UBANGIJI, ka kuma gwada ni,
ka bincike zuciyata da tunanina;
3 gama ƙaunarka kullum tana a gabana,
kuma ina cin gaba da tafiya a cikin gaskiyarka.

4 Ba na zama tare da masu ruɗu,
ko in yi tarayya da masu riya;
5 na ƙi jinin taron masu aikata mugunta
na ƙi in zauna tare da mugaye.
6 Na wanke hannuwana cikin rashin laifi,
ina yawo a bagadenka Ya UBANGIJI,
7 ina shelar yabonka da ƙarfi
ina faɗin dukan ayyukanka masu banmamaki.

8 Ina ƙaunar gidan da kake zama, ya UBANGIJI,
wurin da ɗaukakarka ke zaune.
9 Kada ka ɗauke raina tare da masu zunubi
raina tare da masu son yin kisankai
10 waɗanda akwai mugayen dabaru a hannuwansu,
waɗanda hannuwansu na dama suna cike da cin hanci.
11 Amma na yi rayuwa marar zargi;
ka cece ni ka kuma yi mini jinƙai.

12 Kafafuna suna tsaye daram;
cikin taro mai girma zan yabi UBANGIJI.

# Zabura 27

Ta Dawuda.
1 UBANGIJI ne haskena da cetona,
wa zan ji tsoro?
UBANGIJI ne mafakar raina,
wane ne zan ji tsoro?

2 Sa'ad da mugaye suka tasar mini
don su cinye ni,
sa'ad da abokan gābana da maƙiyina suka kawo mini hari,
sun yi tuntuɓe suka fāɗi.
3 Ko da yake mayaƙa sun kewaye ni,
zuciyata ba za tă ji tsoro ba;
ko da yake ya ɓarke a kaina,
duk da haka zan ƙarfafa.

4 Abu guda na roƙi UBANGIJI,

wannan shi ne na nema,
cewa in zauna a gidan UBANGIJI
dukan kwanakin raina,
in dubi kyan UBANGIJI
in kuma neme shi a cikin haikalinsa.
5 Gama a lokacin wahala,
zai kiyaye ni lafiya a wurin zamansa;
zai ɓoye ni cikin inuwar tabanakul nasa
ya kuma sa ni can a bisa dutse.

6 Sa'an nan kaina zai ɗaukaka
a bisa abokan gābana waɗanda suka kewaye ni;
a tabanakul nasa zan miƙa hadaya da sowa ta farin ciki;
zan rera in kuma yi kiɗi ga UBANGIJI.

7 Ka ji muryata sa'ad da na yi kira, ya UBANGIJI;
ka yi mini jinƙai ka kuma amsa mini.
8 Zuciyata kan faɗa game da kai, "Nemi fuskarsa!"
Fuskarka, UBANGIJI, zan nema.
9 Kada ka ɓoye fuskarka daga gare ni,
kada ka kore bawanka daga gare ka cikin fushi;
kai ne ka kasance mai taimakona.
Kada ka ƙi ni ko ka yashe ni,
Ya Allah Mai cetona.
10 Ko da mahaifina da mahaifiyata sun yashe ni,
UBANGIJI zai karɓe ni.
11 Ka koya mini hanyarka, ya UBANGIJI;
ka bi da ni a miƙaƙƙiyar hanya
saboda masu danne ni.
12 Kada ka ba da ni da sha'awar maƙiyina,
gama masu shaidar ƙarya sun taso a kaina,
suna numfasa tashin hankali.

13 Har yanzu ina da ƙarfin gwiwa a wannan cewa
zan ga alherin UBANGIJI;
a ƙasar masu rai.
14 Ka dogara ga UBANGIJI,
ka yi ƙarfin hali ka yi ƙarfin zuciya
ka kuma dogara ga UBANGIJI.

# Zabura 28

Ta Dawuda.
1 A gare ka nake kira,
ya UBANGIJI Dutsena;
kada ka yi mini kunnen ƙashi.
Gama in ka yi shiru,
zan zama kamar waɗanda suka gangara rami.
2 Ka ji kukata ta neman jinƙai
yayinda nake kira ka don neman taimako,
yayinda nake daga hannuwana
wajen Wurinka Mafi Tsarki.

3 Kada ka ja ni tare da mugaye,
tare da masu yin mugunta,
masu magana kamar ta alheri ce da maƙwabtansu
amma suna riƙe da su a zukatansu.
4 Ka sāka musu da ayyukansu
da kuma don mugun aikinsu;
ka sāka musu saboda abin da hannuwansu suka yi
ka kuma mayar musu abin da ya dace da su.

5 Da yake ba su kula da ayyukan UBANGIJI
da abin da hannuwansa suka yi ba,
zai rushe su
ba kuwa zai ƙara gina su ba.

6 Yabo ya tabbata ga UBANGIJI,
gama ya ji kukata na neman jinƙai.
7 UBANGIJI shi ne ƙarfina da garkuwata;
zuciyata ta amince da shi, kuma na sami taimako.
Zuciyata ta yi tsalle don farin ciki
zan kuwa yi godiya gare shi cikin waƙa.

8 UBANGIJI shi ne ƙarfin mutanensa,
kagarar ceto domin shafaffensa.
9 Ka cece mutanenka ka kuma albarkace gādonka;
ka zama mai kiwonsu ka kuma riƙe su har abada.

# Zabura 29

Zabura ta Dawuda.
1 Ku ba da girma ga UBANGIJI, ya ku manya,
ku ba da girma ga UBANGIJI saboda ɗaukaka da kuma ƙarfinsa.
2 Ku ba da girma ga UBANGIJI, ɗaukakar da ta dace da sunansa;
ku bauta wa UBANGIJI cikin ɗaukakar tsarkinsa.

3 Muryar UBANGIJI tana a bisa ruwaye;
Allah Maɗaukaki ya yi tsawa,
UBANGIJI ya yi tsawa a bisa manyan ruwaye.
4 Muryar UBANGIJI mai iko ce;
muryar UBANGIJI da girma take.
5 Muryar UBANGIJI ta kakkarya itatuwan al'ul na Lebanon.
UBANGIJI ya kakkarya itatuwan al'ul na Lebanon kucu-kucu.
6 Ya sa dutsen Lebanon ya yi ta tsalle kamar ɗan maraƙi,
Siriyon* kuma kamar ɗan jakin jeji.
7 Muryar UBANGIJI ta buga
da walƙatar walƙiya.
8 Muryar UBANGIJI ta girgiza hamada
UBANGIJI ya girgiza Hamadan Kadesh.
9 Muryar UBANGIJI ta murɗa itatuwan oak†
ya kakkaɓe itatuwan kurmi.
Kuma a cikin haikalinsa kowa ya ce, "Daukaka!"

* **Zabura 29:6** Wato, Dutsen Hermon † **Zabura 29:9** Ko kuwa UBANGIJI ya sa barewa ta haihu.

10 UBANGIJI na zaune yana sarauta a bisa rigyawa;
UBANGIJI yana sarauta kamar Sarki har abada.
11 UBANGIJI kan ba da ƙarfi ga mutanensa;
UBANGIJI kan albarkace mutanensa da salama.

# Zabura 30

Zabura ce. Wata waƙa. Don keɓewar haikali.* Ta Dawuda.
1 Zan girmama ka Ya UBANGIJI,
gama ka tsamo ni daga zurfafa
ba ka bar abokan gābana sun yi farin ciki a kaina ba.
2 Ya UBANGIJI Allahna, na yi kira gare ka don taimako
ka kuwa warkar da ni.
3 Ya UBANGIJI, ka dawo da ni daga kabari;
ka kiyaye ni daga gangarawa zuwa cikin rami.

4 Ku rera ga UBANGIJI, ku tsarkakansa;
ku yabi sunansa mai tsarki.
5 Gama fushinsa na ɗan lokaci ne
amma alherinsa har matuƙa ne;
mai yiwuwa a yi kuka da dare
amma farin ciki kan zo da safe.

6 Sa'ad da nake lafiya, na ce,
"Ba zan jijjigu ba."
7 Ya UBANGIJI, sa'ad da ka yi mini alheri,
ka sa katangar dutsena ya tsaya daram;
amma sa'ad da ka ɓoye fuskarka,
sai in cika da tsoro.

8 A gare ka, ya UBANGIJI, na yi kira;
a gare ka Ubangiji na yi kukan neman jinƙai.
9 "Wace riba ce a hallakata,
a kuma gangarawa ta zuwa cikin rami?
Kura za tă yabe ka ne?
Za tă iya yin shelar amincinka?
10 Ka ji, ya UBANGIJI, ka kuwa yi mini jinƙai;
Ya UBANGIJI, ka zama taimakona."

11 Ka mai da kukata ta zama rawa;
ka tuɓe rigar makokina ka sa mini na farin ciki,
12 don zuciyata za tă iya rera gare ka ba kuwa za tă yi shiru ba.
Ya UBANGIJI Allahna, zan yi maka godiya har abada.

# Zabura 31

Don mai bi da kaɗe-kaɗe. Zabura ta Dawuda.
1 A gare ka, ya UBANGIJI, na nemi mafaka;
kada ka bari in taɓa shan kunya;
ka cece ni cikin rahamarka.
2 Ka juye kunnenka gare ni,
ka zo da sauri ka cece ni;
ka zama dutsen mafakata,

* **Zabura 30:** Kan magana, ko kuwa faɗa

mafaka mai ƙarfi na cetona.
3 Da yake kai ne dutsena da kuma kagarata,
saboda sunanka ka bi da ni ka kuma jagorance ni.
4 Ka ʼyantar da ni daga tarkon da aka sa mini,
gama kai ne mafakata.
5 Cikin hannuwanka na miƙa ruhuna;
ka cece ni, ya UBANGIJI Allah na gaskiya.

6 Na ƙi waɗanda suke manne wa gumakan banza;
na dogara ga UBANGIJI.
7 Zan yi murna in kuma yi farin ciki a cikin ƙaunarka,
gama ka ga azabata
ka kuma san wahalar raina.
8 Ba ka ba da ni ga abokin gāba ba
amma ka sa ƙafafuna a wuri mai sarari.

9 Ka yi mini jinƙai, ya UBANGIJI, gama ina cikin damuwa;
idanuna sun gaji da baƙin ciki,
raina da jikina sun tafke tilis.
10 Baƙin ciki ya rufe raina
shekaruna sun cika da nishi;
ƙarfina ya karai saboda azaba,
ƙasusuwana kuma sun gaji tiƙis.
11 Saboda dukan abokan gābana,
Na zama tamƙar abin reni na maƙwabtana;
na zama abin tsoro ga abokaina,
waɗanda suka gan ni a titi sukan gudu daga gare ni.
12 An manta da ni sai ka ce na mutu;
na zama kamar fasasshen kasko.
13 Gama nakan ji raɗe-raɗen mutane masu yawa;
akwai tsoro a kowane gefe;
suna ƙulla maƙarƙashiya a kaina
suna shirya su ɗauke raina.

14 Amma na dogara gare ka, ya UBANGIJI;
na ce, “Kai ne Allahna.”
15 Lokutana suna a hannuwanka;
ka cece ni daga abokan gābana
da kuma daga waɗanda suke fafara ta.
16 Bari fuskarka ta haskaka a kan bawanka;
ka cece ni da ƙaunarka marar ƙarewa.
17 Kada ka bari in sha kunya, ya UBANGIJI,
gama na yi kuka gare ka;
amma bari mugaye su sha kunya
su kuma kwanta shiru a cikin kabari.
18 Bari a rufe leɓunan ƙarairayinsu,
gama da fariya da reni
suna magana da girman kai a kan adalai.

19 Alherinka da girma yake,
wanda ka ajiye domin waɗanda suke tsoronka,
wanda ka mayar a gaban mutane

a kan waɗanda suke neman mafaka daga gare ka.
20 Cikin inuwar kasancewarka ka ɓoye su
daga makircin mutane;
a wurin zamanka ka kiyaye su lafiya
daga harsuna masu zagi.

21 Yabo ya tabbata ga UBANGIJI,
gama ya nuna ƙaunarsa mai banmamaki gare ni
sa'ad da aka yi mini kwanto kewaye da birni.
22 Cikin tsorona na ce,
"An yanke ni daga gabanka!"
Duk da haka ka ji kukata na neman jinƙai
sa'ad da na kira gare ka don taimako.

23 Ku ƙaunaci UBANGIJI, dukanku tsarkakansa!
UBANGIJI yakan adana amintattu,
amma masu girman kai yakan sāka musu cikakke.
24 Ku yi ƙarfin hali ku kuma ƙarfafa,
dukanku masu sa bege a kan UBANGIJI.

# Zabura 32

Ta Dawuda. *Maskil** ne.
1 Mai farin ciki ne shi
wanda aka gafarta masa laifofinsa,
wanda aka shafe zunubansa.
2 Mai farin ciki ne mutumin
da UBANGIJI ba ya lissafin zunubinsa a kansa
wanda kuma babu ruɗu a ruhunsa.

3 Sa'ad da na yi shiru,
ƙasusuwana sun yi ta mutuwa
cikin nishina dukan yini.
4 Gama dare da rana
hannunka yana da nauyi a kaina;
an shanye ƙarfina ƙaf
sai ka ce a zafin bazara.

Sela

5 Sa'an nan na furta zunubina a gare ka
ban kuwa ɓoye laifina ba.
Na ce, "Zan furta
laifofina ga UBANGIJI."
Ka kuwa gafarta
laifin zunubina.

Sela

6 Saboda haka bari duk mai tsoron Allah yă yi addu'a gare ka
yayinda kake samuwa;
tabbatacce sa'ad da manyan ruwaye suka taso,
ba za su kai wurinsa ba.
7 Kai ne wurin ɓuyata;

* **Zabura 32:** Kan magana, mai yiwuwa wata kalmar kiɗi ce.

za ka tsare ni daga wahala
ka kewaye ni da waƙoƙin ceto.

Sela

8 Zan umarce ka in kuma koyar da kai a hanyar da za ka bi;
Zan ba ka shawara in kuma lura da kai.
9 Kada ka zama kamar doki ko doki,
wanda ba su da azanci
wanda dole sai an bi da su da linzami da ragama
in ba haka ba, ba za su zo wurinka ba.
10 Azaban mugu da yawa suke,
amma ƙaunar UBANGIJI marar ƙarewa
kan kewaye mutumin da ya dogara gare shi.

11 Ku yi farin ciki a cikin UBANGIJI ku kuma yi murna, ku adalai;
ku rera, dukanku waɗanda zuciyarku take daidai!

# Zabura 33

1 Ku rera da farin ciki ga UBANGIJI ku adalai;
daidai ne masu gaskiya su yabe shi.
2 Ku yabi UBANGIJI da garaya;
ku yi kiɗi gare shi da molo mai tsirkiya goma.
3 Ku rera masa sabuwar waƙa;
ku yi kiɗi da gwaninta, ku kuma yi sowa don farin ciki.

4 Gama maganar UBANGIJI daidai ne da kuma gaskiya;
yana da aminci cikin kome da yake yi.
5 UBANGIJI yana ƙaunar adalci
duniya ta cika da ƙaunarsa marar ƙarewa.

6 Ta wurin maganar UBANGIJI aka yi sammai,
rundunar taurarinsu kuwa da numfashin bakinsa.
7 Ya tattara ruwan teku cikin tuluna;*
ya sa zurfafa cikin gidajen ajiya.
8 Bari dukan duniya ta ji tsoron UBANGIJI;
bari dukan mutanen duniya su girmama shi.
9 Gama ya yi magana, abu ya kuwa kasance;
ya umarta, ya kuwa tsaya daram.

10 UBANGIJI yakan soke shirye-shiryen al'ummai;
yakan wofintar da manufofin mutane.
11 Amma shirye-shiryen UBANGIJI kan tsaya daram har abada,
manufofin zuciyarsa kuwa har dukan zamanai.

12 Mai farin ciki ce al'ummar da Allah ne UBANGIJINTA,
mutanen da ya zaɓa don gādonsa.
13 Daga sama UBANGIJI ya duba
ya kuwa ga dukan 'yan adam;
14 daga mazauninsa yana lura
da dukan waɗanda suke zama a duniya,

* **Zabura 33:7** Ko kuwa teku sai ka ce a tsibi

15 shi da ya yi zukatan duka,
wanda yake kula da kome da suke yi.

16 Babu sarkin da ake ceto ta wurin yawan mayaƙansa;
ba jarumin da kan kuɓuta ta wurin yawan ƙarfinsa.
17 Dogara a kan doki don ceto banza ne;
duk da yawan ƙarfinsa ba ya ceto.
18 Amma idanun UBANGIJI suna a kan wanda yake tsoronsa,
a kan waɗanda suke sa zuciya cikin ƙaunarsa marar ƙarewa,
19 don yă cece su daga mutuwa
ya bar su da rai a lokacin yunwa.

20 Muna jiran UBANGIJI da bege;
shi ne taimakonmu da garkuwarmu.
21 A cikinsa zukatanmu na farin ciki,
gama mun dogara cikin sunansa mai tsarki.
22 Bari ƙaunarka marar ƙarewa ta zauna a kanmu, ya UBANGIJI,
ko ma da muke sa begenmu a gare ka.
*

# Zabura 34

Ta Dawuda. Sa'ad da ya yi kamar ya haukace a gaban Abimelek, Wanda ya kore shi, ya kuwa tafi.

1 Zan gode wa UBANGIJI kullayaumi;
yabonsa kullum za su kasance a leɓunana.
2 Raina zai yi fariya a cikin UBANGIJI;
bari waɗanda suke wahala su ji su kuma yi farin ciki.
3 Ku ɗaukaka UBANGIJI tare da ni;
bari mu ɗaukaka sunansa tare.

4 Na nemi UBANGIJI, ya kuwa amsa mini;
ya cece ni daga dukan tsoro.
5 Waɗanda suke dubansa sukan haskaka;
fuskokinsu ba sa rufuwa da kunya.
6 Wannan matalauci ya yi kira, UBANGIJI kuwa ya ji shi;
ya cece shi daga dukan wahalarsa.
7 Mala'ikan UBANGIJI ya kafa sansani kewaye da waɗanda suke tsoronsa,
ya kuwa cece su.

8 Ku gwada ku gani cewa UBANGIJI yana da kyau;
mai albarka ne mutumin da yake neman mafaka a gare shi.
9 Ku ji tsoron UBANGIJI, ku tsarkakansa,
gama masu tsoronsa ba sa rasa kome.
10 Zakoki za su iya rasa ƙarfi su kuma ji yunwa,
amma waɗanda suke neman UBANGIJI ba sa rasa abu mai kyau.
11 Ku zo, 'ya'yana, ku saurare ni;
zan koya muku tsoron UBANGIJI.
12 Duk waninku da yake ƙaunar rayuwa
yana kuma so yă ga kwanaki masu kyau,

* **Zabura 34:** Wannan zabura waƙa ce, mai ayoyin da suka fara da harufan Ibraniyanci bi da bi.

13 ka kiyaye harshenka daga mugunta
da kuma leɓunanku daga faɗar ƙarairayi.
14 Juyo daga mugunta ku yi alheri;
nemi salama ku kuma yi ƙoƙarin samunta.

15 Idanun UBANGIJI suna a kan masu adalci
kuma kunnuwansa suna sauraran kukansu;
16 fuskar UBANGIJI yana gāba da waɗanda suke aikata mugunta,
don yă sa a manta da su a duniya.

17 Adalai kan yi kuka, UBANGIJI kuwa yakan ji su;
yakan cece su daga dukan wahalarsu.
18 UBANGIJI yana kusa da waɗanda suka karai
ya kuma cece waɗanda aka ragargaza a ruhu.

19 Adali zai iya kasance da wahala da yawa,
amma UBANGIJI yakan cece shi daga dukansu;
20 yakan tsare dukan ƙasusuwansa,
ba ko ɗayansu da zai karye.

21 Mugunta zai kashe mugu;
za a hukunta abokan gāban adalai.
22 UBANGIJI yakan cece bayinsa;
ba wanda yake neman mafaka a wurinsa da za a hukunta.

# Zabura 35

Ta Dawuda.
1 Yi hamayya, ya UBANGIJI, da waɗanda suke hamayya da ni;
yi faɗa da waɗanda suke faɗa da ni.
2 Ka ɗauki garkuwa da kuma makami;
ka tashi ka taimake ni.
3 Ka ɗaga māshi da kuma abin da ake jefa*
a kan waɗanda suke fafarata.
Ka ce wa raina,
"Ni ne cetonka."

4 Bari waɗanda suke neman raina
su sha kunya a kuma kunyatar da su;
bari waɗanda suke shirya lalacewata
su juya da baya su ruɗe.
5 Bari su zama kamar yayi a gaban iska,
mala'ikan UBANGIJI kuma yana korarsu;
6 bari hanyarsu tă yi duhu ta kuma yi santsi,
mala'ikan UBANGIJI kuma yana fafararsu.

7 Da yake sun ɓoye tarko domina ba dalili
kuma babu dalili suka haƙa mini rami,
8 bari lalaci yă kama su ba zato,
bari tarkon da suka ɓoye yă kama su,
bari su fāɗa cikin ramin, yă kai ga lalacinsu.

---
* **Zabura 35:3** Ko kuwa ka kuwa tare hanya

9 Sa’an nan raina zai cika da farin ciki a cikin UBANGIJI
in yi kuma murna a cikin cetonsa.
10 Dukan raina zai ce,
“Wane ne kamar ka, ya UBANGIJI?
Ka kuɓutar da matalauta daga waɗanda suka fi ƙarfinsu,
matalauta da masu bukata daga waɗanda suke musu fashi.”

11 Shaidu marasa imani sun fito;
suna mini tambaya a kan abubuwan da ban san kome a kai ba.
12 Suna sāka alherin da na yi musu da mugunta
suka bar raina da nadama.
13 Duk da haka sa’ad da suke ciwo, na sanya rigar makoki
na ƙasƙantar da kaina da azumi.
Sa’ad da aka mayar mini da addu’o’i babu amsa,
14 nakan yi ta yawo ina makoki
sai ka ce yadda nake yi wa abokina ko ɗan’uwana.
Nakan sunkuyar da kaina cikin baƙin ciki
sai ka ce ina kuka domin mahaifiyata.
15 Amma sa’ad da na yi tuntuɓe, sukan taru suna murna;
masu kai hari sun taru a kaina sa’ad da ban sani ba.
Suna ɓata mini suna ba tsagaitawa.
16 Kamar marasa sani Allah suna mini riyar ba’a;
Suna hararata da ƙiyayya.

17 Ya UBANGIJI, har yaushe za ka ci gaba da zuba ido kawai?
Ka kuɓutar da raina daga farmakinsu,
raina mai daraja daga waɗannan zakoki.
18 Zan yi godiya cikin taro mai girma;
cikin ɗumbun mutane zan yabe ka.
19 Kada ka bar maƙaryatan nan,
su yi farin ciki a kaina;
kada ka bar waɗanda suke ƙina ba dalili,
su ji daɗin baƙin cikina.
20 Ba sa maganar salama
sukan ƙirƙiro zage-zagen ƙarya
a kan waɗanda suka zama shiru a ƙasar.
21 Sukan wage mini bakinsu suna cewa, “Allah yă ƙara!
Da idanunmu mun gani.”

22 Ya UBANGIJI, ka ga wannan; kada ka yi shiru.
Kada ka yi nisa da ni, ya Ubangiji.
23 Ka farka, ka kuma tashi ka kāre ni!
Ka yi mini faɗa, ya Allahna da shugabana.
24 Ka nuna ni marar laifi ne ciki adalcinka,
Ya UBANGIJI Allahna; kada ka bari su yi farin ciki a kaina.
25 Kada ka bari su ce wa kansu, “Allah yă ƙara, dā ma abin da mun so ke nan!”
Ko su ce, “Mun haɗiye shi.”

26 Bari dukan waɗanda suke farin ciki a kaina a wahalata
su sha kunya su kuma ruɗe;
bari dukan waɗanda suke ɗaukar kansu sun fi ni
su sha kunya da wulaƙanci.

27 Bari waɗanda suke murna saboda nasarata
su yi sowa don farin ciki da murna;
bari kullum su riƙa cewa, “A ɗaukaka UBANGIJI,
wanda yake farin ciki da zaman lafiyar bawansa.”

28 Harshena zai yi zancen adalcinka
da kuma yabonka dukan yini.

# Zabura 36

Don mai bi da kaɗe-kaɗe. Ta Dawuda bawan UBANGIJI.
1 Akwai magana a cikin zuciyata
game da zunubin mugu.
Babu tsoron Allah
a idanunsa.

2 Gama a idanunsa yana ganin kansa wani abu ne
wanda ya sha ƙarfi a gane ko ya ƙi zunubinsa.
3 Kalmomin bakinsa mugaye ne da kuma ruɗu;
ya daina zama mai hikima da yin alheri.
4 Ko a kan gadonsa ma yana shirya mugunta;
yakan sa kansa ga aikata zunubi
kuma ba ya ƙin abin da ba shi da kyau.

5 Kaunarka, ya UBANGIJI, kan kai sammai,
amincinka har sararin sammai.
6 Adalcinka yana kama da manyan duwatsu,
hukuncinka kamar zurfi mai girma.
Ya UBANGIJI, kana lura da mutum da dabba.
7 Ina misalin ƙaunarka marar ƙarewa!
Mutane manya da ƙanana kan sami mafaka cikin inuwar fikafikanka.
8 Suna biki a yalwar gidanka;
kakan ba su sha daga rafin farin cikinka.
9 Gama a gare ka akwai maɓulɓular rai
cikin haskenka mukan ga haske.

10 Ka ci gaba da ƙaunarka ga waɗanda suka san ka,
adalcinka ga masu gaskiyar zuciya.
11 Kada ka bari ƙafar mai girman kai yă fāɗa mini,
ko hannun mugu ya kore ni.
12 Dubi yadda masu aikata zunubi suka fāɗi,
a zube, ba za su kuwa iya tashi ba!
*

# Zabura 37

Ta Dawuda.
1 Kada ka tsorata saboda mugayen mutane
ko ka yi kishin waɗanda suka aikata mugunta;
2 gama kamar ciyawa za su bushe,
kamar ɗanyun ganyaye za su mutu.

* **Zabura 37:** Wannan zabura waƙa ce, mai ayoyin da suka fara da harufan Ibraniyanci bi da bi.

3 Ka dogara ga UBANGIJI ka kuma aikata alheri;
yi zama cikin ƙasar ka kuma more makiyaya mai lafiya.
4 Ka ji daɗinka a cikin UBANGIJI
zai kuwa biya bukatun zuciyarka.

5 Ka sa kanka a hanyar UBANGIJI;
ka kuma dogara gare shi zai kuwa yi wannan.
6 Zai sa adalcinka yǎ haskaka kamar hasken safiya,
gaskiyarka kuma kamar rana a tsaka.

7 Ka natsu a gaban UBANGIJI
ka kuma jira da haƙuri gare shi;
kada ka tsorata sa'ad da mutane ke nasara a hanyoyinsu,
sa'ad da suke aikata mugayen shirye-shiryensu.

8 Kada ka yi fushi kada kuma ka yi hasala;
kada ka tsorata, wannan yakan kai ga mugunta ne kawai.
9 Gama za a datse mugayen mutane,
amma waɗanda suke sa zuciya ga UBANGIJI za su gāji ƙasar.

10 A ɗan ƙanƙanen lokaci, mugaye za su shuɗe;
ko ka neme su, ba za a same su ba.
11 Amma masu tawali'u za su gāji ƙasar
su kuma zauna da cikakkiyar salama.

12 Mugaye sukan shirya wa adalai maƙarƙashiya
su ciji baki a kansu;
13 amma Ubangiji yakan yi dariyar mugaye,
gama ya sani ranarsu tana zuwa.

14 Mugaye sukan zare takobi
su ja baka
don su kashe matalauta da masu bukata,
don su kashe waɗanda hanyoyinsu daidai suke.
15 Amma takubansu za su soki zukatansu,
kuma bakkunansu za su kakkarye.

16 Kanƙanen abin da mai adalci yake da shi
ya fi arzikin mugaye yawa;
17 gama za a kakkarya ikon mugaye,
amma UBANGIJI zai riƙe mai adalci.

18 Kwanakin marasa zarge suna sane ga UBANGIJI,
kuma gādonsu zai dawwama har abada.
19 A lokutan masifu ba za su yanƙwane ba;
a kwanakin yunwa za su sami a yalwace.

20 Amma mugaye za su hallaka,
Abokan gāban UBANGIJI za su zama kamar kyan gonaki,
za su ɓace, za su ɓace kamar hayaƙi.

21 Mugaye kan yi rance ba sa kuma biya,
amma masu adalci suna bayar hannu sake;
22 waɗanda UBANGIJI ya sa wa albarka za su gāji ƙasar,
amma waɗanda ya la'anta, za a kore su.

23 In UBANGIJI ya ji daɗin hanyar da mutum yake bi,
zai sa sawu su kahu;
24 ko ya yi tuntuɓe, ba zai fāɗi ba,
gama UBANGIJI yakan riƙe shi da hannunsa.

25 Dā ni yaro ne amma yanzu na tsufa,
duk da haka ban taɓa ganin an yashe masu adalci ba
ko a ce 'ya'yansu suna roƙon burodi.
26 Kullum suna bayar hannu sake suna kuma ba da bashi ba da wahala ba,
za a yi wa 'ya'yansu albarka.

27 Ku juyo daga mugunta ku yi alheri;
sa'an nan za ku zauna a ƙasar har abada.
28 Gama UBANGIJI yana ƙaunar masu aikata daidai
kuma ba zai yashe amintattunsa ba.

Za a hallaka masu aikata mugunta gaba ɗaya,
'ya'yan mugaye za su hallaka.
29 Masu adalci za su gāji ƙasar
su kuma zauna a cikinta har abada.

30 Bakin mutum mai adalci yakan yi magana da hikima,
harshensa kuwa yakan yi maganar abin da yake daidai.
31 Dokar Allahnsa tana a cikin zuciyarsa;
ƙafafunsa ba sa santsi.

32 Mugaye suna fako suna jira masu adalci,
suna ƙoƙari neman ransu;
33 amma UBANGIJI ba zai bar su a ikonsu ba
ko ya bari a hukunta su sa'ad da aka kawo su shari'a ba.

34 Ku sa zuciya ga UBANGIJI
ku kuma kiyaye hanyarsa.
Zai ɗaukaka ku ku ci gādon ƙasar,
sa'ad da aka kawar da mugaye, za ka gani.

35 Na ga wani mugu, azzalumi,
yana yaɗuwa kamar ɗanyen itace a asalin ƙasarsa,
36 amma yakan mutu nan da nan kuma ba ya ƙara kasancewa;
ko an neme shi, ba za a same shi ba.

37 Ka dubi marasa zargi, ka lura da adali;
akwai sa zuciya domin mutum mai salama.
38 Amma za a hallaka dukan masu zunubi;
za a yanke sa zuciya ta mugaye.

39 Ceton adalai kan zo daga UBANGIJI;
shi ne mafaka a lokacin wahala.
40 UBANGIJI yakan taimake su yǎ kuma cece su;
yakan kuɓutar da su daga mugaye yǎ kuma cece su,
domin sukan nemi mafaka daga gare shi.

# Zabura 38

Zabura ta Dawuda. Roƙo ne.
1 Ya UBANGIJI, kada ka tsawata mini cikin fushinka
ko ka hore ni cikin hasalarka.
2 Gama kibiyoyinka sun soke ni,
hannunka kuma ya fāɗo a kaina.
3 Saboda hasalarka babu lafiya a jikina;
ƙasusuwana ba lafiya saboda zunubina.
4 Laifofina sun mamaye ni
kamar nauyin da ya sha ƙarfin ɗauka.

5 Miyakuna sun ruɓe suna kuma wari
saboda wawancina na zunubi.
6 An tanƙware ni aka kuma ƙasƙantar da ni;
dukan yini ina ta kuka.
7 Bayana yana fama da zazzaɓi;
babu lafiya a jikina.
8 Na gaji sharkaf an kuma ragargaza ni;
ina nishi da wahala a cikin zuciyata.

9 Dukan bukatata tana a shimfiɗe a gabanka, ya Ubangiji;
ajiyar zuciyata ba ta ɓoyuwa daga gare ka.
10 Zuciyata na bugu, ƙarfina kuma ya ƙare,
har ma haske ya rabu da idanuna.
11 Abokaina da maƙwabtana sun guje ni saboda miyakuna;
maƙwabtana ba sa zuwa kusa.
12 Waɗanda suke neman raina sun sa tarkonsu,
waɗanda suke so su cuce ni suna zance lalatar da ni;
yini sukutum suna ƙulla mini maƙarƙashiya.

13 Ni kamar kurma ne, wanda ba ya ji,
kamar bebe, wanda ba ya iya buɗe bakinsa.
14 Na zama kamar mutumin da ba ya ji,
wanda bakinsa ba ya iya ba da amsa.
15 Na dogara gare ka, ya UBANGIJI;
za ka amsa, ya Ubangiji Allahna.
16 Gama na ce, “Kada ka bar su su yi farin ciki a kaina
ko su yi kirari a kaina sa'ad da ƙafata ta yi santsi.”

17 Gama ina gab da fāɗuwa,
kuma cikin azaba nake kullum.
18 Na furta laifina;
na damu da zunubina.
19 Da yawa ne masu gāba da ni da ƙarfi;
waɗanda suke kina ba dalili sun yi yawa.
20 Waɗanda suke sāka alherina da mugunta,

suna cin zarafina
sa'ad da nake bin abin da yake daidai.

21 Ya UBANGIJI, kada ka yashe ni;
kada ka yi nesa da ni, ya Allahna.
22 Zo da sauri ka taimake ni,
Ya Ubangiji Mai Cetona.

# Zabura 39

Don mai bi da kaɗe-kaɗe. Don Yedutun. Zabura ta Dawuda.
1 Na ce, "Zan lura da hanyoyina
zan kuma kiyaye harshena daga zunubi;
zan sa linzami a bakina
muddin mugaye suna a gabana."
2 Na yi shiru, ban ce kome ba,
Ko a kan abin da yake da kyau!
Amma duk da haka wahalata sai ƙaruwa take yi;
3 zuciyata ta ƙara zafi a cikina.
Kuma sa'ad da nake tunani, wuta ta yi ta kuna;
sai na yi magana da harshena na ce,

4 "Nuna mini, ya UBANGIJI, ƙarshen rayuwata
da kuma yawan kwanakina;
bari in san yadda rayuwata tana wucewa da sauri.
5 Ka sa kwanakina suka zama tafin hannu ne kawai;
yawan shekaruna kamar ba kome ba ne a gabanka.
Duk ran mutum shaƙar iska ne kurum,
har ma waɗanda suke tsammani suke da kāriya.
Sela

6 "Mutum dai shirim ne kawai yayinda yake kai da komowa.
Yana ta yawo, amma a banza ne kawai;
yakan tara dukiya, ba tare da sanin wa zai more ta ba.

7 "Amma yanzu, ya Ubangiji, me zan nema?
Begena yana a gare ka.
8 Ka cece ni daga dukan laifofina;
kada ka sa in zama abin dariya ga wawaye.
9 Na yi shiru; ba zan buɗe bakina ba,
gama kai ne wanda ka aikata wannan.
10 Ka ɗauke bulalarka daga gare ni;
na ji jiki ta wurin bugun da hannunka ya yi mini.
11 Kakan tsawata ka kuma hore mutane saboda zunubinsu;
kakan cinye wadatarsu kamar yadda asu ke yi,
kowane mutum dai shaƙar iska ne.
Sela

12 "Ka ji addu'ata, ya UBANGIJI,
ka saurari kukata ta neman taimako;
kada ka kurmance ga kukata.
Gama ina zama tare da kai kamar baƙo,
baƙo, kamar yadda dukan kakannina sun kasance.

13 Ka kau da fuskarka daga gare ni, saboda in sāke yin farin ciki
kafin in tafi in kuma rabu da nan.”

# Zabura 40

Don mai bi da kaɗe-kaɗe. Ta Dawuda. Zabura ce.
1 Na jira da haƙuri ga UBANGIJI;
ya juya wurina ya kuma ji kukata.
2 Ya ɗaga ni daga rami marar fāɗi,
daga laka da taɓo;
ya sa ƙafafuna a kan dutse
ya kuma ba ni tsayayyen wuri don in tsaya.
3 Ya sa sabuwar waƙa a bakina,
waƙar yabo ga Allahna.
Da yawa za su gani su tsorata
su kuma dogara ga UBANGIJI.

4 Mai albarka ne mutumin
da ya mai da UBANGIJI abin dogararsa,
wanda ba ya kula da masu girman kai,
waɗanda suka juya ga allolin ƙarya.
5 Da yawa ne, ya UBANGIJI Allahna,
abubuwan banmamakin da ka aikata.
Abubuwan da ka shirya mana.
Ba wanda zai iya faɗa maka su;
a ce zan yi magana in faɗe su,
za su wuce gaban misali a furta.

6 Hadaya da sadaka ba ka sha’awa,
amma kunnuwana ka huda;
hadayun ƙonawa da hadayun zunubi ba ka bukata.
7 Sa’an nan na ce, “Ga ni, na zo,
kamar yadda yake a rubuce game da ni cikin littafi.
8 Ina sha’awar aikata nufinka, ya Allahna;
dokar tana cikin zuciyata.”

9 Na yi shelar adalcinka cikin babban taro;
ba na rufe leɓunana,
kamar yadda ka sani, ya UBANGIJI.
10 Ba na ɓoye adalcinka cikin zuciyata;
ina maganar amincinka da cetonka.
Ban ɓoye ƙaunarka da gaskiyarka
a gaban taron jama’arka mai girma ba.

11 Kada ka hana mini jinƙanka, ya UBANGIJI;
bari ƙaunarka da gaskiyarka kullum su kāre ni.
12 Gama damuwoyin da suka wuce misali sun kewaye ni;
zunubaina sun mamaye ni, kuma ba na iya gani.
Sun fi gashin kaina yawa,
har ma na fid da zuciya.
13 Ka ji daɗin cetona, ya UBANGIJI;
Ya UBANGIJI, ka zo da sauri ka taimake ni.

14 Bari masu neman raina
su sha kunya su kuma rikice;
bari dukan waɗanda suke neman lalacewata
su koma baya da kunya.
15 Bari masu ce mini, “Allah yă ƙara!”
Su sha mamaki saboda kunyar da za su sha.
16 Amma bari dukan masu nemanka
su yi farin ciki su kuma yi murna a cikinka;
bari waɗanda suke ƙaunar cetonka kullum su ce,
“Ubangiji mai girma ne!”

17 Ni dai matalauci ne da mai bukata;
bari Ubangiji yă tuna da ni.
Kai ne taimakona da mai cetona;
Ya Allahna, kada ka jinkirta.

# Zabura 41

Don mai bi da kaɗe-kaɗe. Zabura ta Dawuda.
1 Mai albarka ne wanda yake jin tausayin marasa ƙarfi;
Ubangiji yakan kuɓutar da shi a lokutan wahala.
2 Ubangiji zai kāre shi yă kuma kiyaye ransa;
zai albarkace shi a cikin ƙasar
ba kuwa zai miƙa shi ga hannun maƙiyansa ba.
3 Ubangiji zai ba shi ƙarfi a gadon rashin lafiyarsa
ya mayar masa da lafiya daga ciwon da ya kwantar da shi.

4 Na ce, “Ya Ubangiji, ka yi mini jinƙai;
ka warkar da ni, gama na yi maka zunubi.”
5 Abokan gābana suna muguwar magana a kaina cewa,
“Yaushe zai mutu sunansa yă ɓace ne?”
6 Duk sa’ad da wani ya zo ganina,
yakan yi maganar ƙarya, yayinda zuciyarsa tana tattare da cin zarafi;
sa’an nan yă fita yă yi ta bazawa ko’ina.

7 Dukan abokan gābana suna raɗa tare a kaina;
suna fata mugun abu ya same ni, suna cewa,
8 “Mugun ciwo ya kama shi;
ba zai taɓa tashi daga inda yake kwanciya ba.”
9 Har abokina na kurkusa,
wanda na amince da shi,
wanda muke cin abinci tare,
ya juya yana gāba da ni.

10 Amma kai, ya Ubangiji, ka yi mini jinƙai,
ka tā da ni, don in sāka musu.
11 Na sani kana jin daɗina,
gama abokin gābana ba zai ci nasara a kaina ba.
12 Cikin mutuncina ka riƙe ni
ka sa ni a gabanka har abada.

13 Yabo ya tabbata ga Ubangiji, Allah na Isra’ila,

har abada abadin.

Amin kuma Amin.

# LITTAFI NA BIYU

## 42

*Zabura 42–72* *

Don mai bi da kaɗe-kaɗe. *Maskil*† ne na ʼYaʼyan Kora maza.

1 Kamar yadda barewa take marmarin ruwan rafuffuka,
haka raina yake marmarinka, ya Allah.
2 Raina yana ƙishin Allah, Allah mai rai.
Yaushe zan tafi in sadu da Allah ne?
3 Hawayena ne sun zama abincina
dare da rana,
yayinda mutane suke ce da ni dukan yini,
"Ina Allahnka ɗin?"
4 Waɗannan abubuwa ne nakan tuna
saʼad da nake faɗin abin da yake a raina,
yadda dā nakan tafi tare da taron jamaʼa,
ina bishe su a jere zuwa gidan Allah,
da sowa ta farin ciki da kuma godiya
a cikin taron biki.

5 Me ya sa kake baƙin ciki, ya raina?
Me ya sa ka damu a cikina?
Ka dogara ga Allah,
gama zai sāke yabe shi,
Mai Cetona da kuma Allahna.

6 Raina‡ yana baƙin ciki a cikina;
saboda haka zan tuna da kai
daga ƙasar Urdun,
a ƙwanƙolin Hermon, daga Dutsen Mizar.
7 Zurfi kan kira zurfi
cikin rurin matsirgar ruwanka;
dukan raƙuma da igiyoyi
sun sha kaina.

8 Da rana UBANGIJI yakan nuna ƙaunarsa,
da dare waƙarsa tana tare da ni,
adduʼa ga Allah na raina.

9 Na ce wa Allah Dutsena,
"Me ya sa ka manta da ni?
Me zai sa in yi ta yawo ina makoki,
a danne a hannun abokin gāba?"
10 Kasusuwana suna jin jiki da wahala
yayinda maƙiyana suna mini baʼa,
suna ce mini dukan yini,
"Ina Allahnka ɗin?"

---

* **Zabura 42:** Cikin rubuce-rubucen hannu na Ibraniyanci masu yawa Zabura 42 da 43, zabura guda ce. † **Zabura 42:** Kan magana, mai yiwuwa wata kalmar waƙa ce. ‡ **Zabura 42:6** Kaɗan a cikin rubuce-rubucen hannu na Ibraniyanci, Seftuwajin da Siriyak; yawancin rubuce-rubucen hannu na Ibraniyanci yabe shi domin taimakon cetonsa. 6 Ya Allahna, nawa

11 Me ya sa kake baƙin ciki, ya raina?
Me ya sa ka damu a cikina?
Ka dogara ga Allah,
gama zai sāke yabe shi,
Mai Cetona da kuma Allahna.
*

# Zabura 43

1 Ka nuna ni marar laifi ne, ya Allah,
ka kuma nemi hakkina
a kan al'ummai marasa sanin Allah.
Ka kuɓutar da ni daga
masu ruɗu da mugayen mutane.
2 Kai ne Allah mafakata.
Me ya sa ka ƙi ni?
Me zai sa in yi ta yawo ina makoki,
a danne a hannun abokin gāba?
3 Ka aiko da haskenka da gaskiyarka,
bari su bishe ni
bari su kawo ni ga dutsenka mai tsarki,
zuwa wurin da kake zama.
4 Sa'an nan zan tafi bagaden Allah,
ga Allah, farin cikina da murnata.
Zan yabe ka da garaya,
Ya Allah, Allahna.

5 Me ya sa kake baƙin ciki, ya raina?
Me ya sa ka damu a cikina?
Ka dogara ga Allah,
gama zai sāke yabe shi,
Mai Cetona da Allahna.

# Zabura 44

Don mai bi da kaɗe-kaɗe. Ta 'ya'yan Kora maza. *Maskil** ne.
1 Mun ji da kunnuwanmu, ya Allah;
kakanninmu sun faɗa mana
abin da ka aikata a kwanakinsu,
tun dā can.
2 Da hannunka ka kori al'ummai
ka kuma dasa kakanninmu;
ka ragargaza mutanen
ka kuma sa kakanninmu suka haɓaka.
3 Ba da takobinsu ba ne suka ci ƙasar,
ba kuwa ƙarfin hannunsu ne ya ba su nasara ba;
hannun damanka ne, ƙarfin hannunka,
da kuma hasken fuskarka, gama ka ƙaunace su.

4 Kai ne Sarkina da kuma Allahna,
wanda ya ba da nasarori wa Yaƙub.
5 Ta wurinka mun tura abokan gābanmu baya;
ta wurin sunanka muka tattake maƙiyanmu.

---

* **Zabura 43:** Cikin rubuce-rubucen hannu masu yawa a Ibraniyanci Zabura 42 da 43 zabura guda ce.
* **Zabura 44:** Kan magana, mai yiwuwa wata kalmar waƙa ce.

6 Ba na dogara ga bakana,
takobina ba ya kawo nasara;
7 amma kana ba mu nasara a kan abokan gābanmu,
ka sa abokan gābanmu suka sha kunya.
8 A cikin Allah muke fariyarmu dukan yini,
kuma za mu yabi sunanka har abada.
Sela

9 Amma yanzu ka ƙi mu ka kuma ƙasƙantar da mu;
ba ka ƙara fita tare da mayaƙanmu.
10 Ka sa muka gudu a gaban abokin gāba,
kuma abokan gābanmu suka washe mu.
11 Ka ba da mu a cinye kamar tumaki
ka kuma watsar da mu a cikin al'ummai.
12 Ka sayar da mutanenka a kuɗin da bai taka ƙara ya karye ba
babu wata riba daga sayar da su da ka yi.

13 Ka mai da mu abin dariya ga maƙwabtanmu,
abin dariya da reni ga waɗanda suke kewaye da mu.
14 Ka sa muka zama abin ba'a a cikin al'ummai;
mutanen suna kaɗa mana kai.
15 Dukan yini ina cikin wulaƙanci,
fuskata kuma ta rufu da kunya
16 saboda ba'ar waɗanda suke zagi suke kuma ƙina,
saboda abokan gābana, waɗanda suka sha alwashi sai sun yi ramuwa.

17 Dukan wannan ya faru da mu,
ko da yake ba mu manta da kai ba
ko mu kasance masu ƙarya ga alkawarinka.
18 Zukatanmu ba su juya baya;
ƙafafunmu ba su kauce daga hanyarka ba.
19 Amma ka ragargaza mu ka kuma maishe mu abin farautar karnukan jeji
ka kuma rufe mu cikin duhu baƙi ƙirin.

20 Da a ce mun manta da sunan Allahnmu
ko mun miƙa hannuwanmu ga baƙin alloli,
21 da Allah bai gane ba,
da yake ya san asiran zuciya?
22 Duk da haka saboda kai mun fuskanci mutuwa dukan yini;
aka ɗauke mu kamar tumakin da za a yanka.

23 Ka farka, ya Ubangiji! Don me kake barci?
Ta da kanka! Kada ka ƙi mu har abada.
24 Me ya sa ka ɓoye fuskarka
ka manta da azabanmu da kuma danniyar da ake mana?

25 An kai mu ƙasa zuwa ƙura;
jikunanmu sun manne da ƙasa.
26 Ka tashi ka taimake mu;
ka cece mu saboda ƙaunarka marar ƙarewa.

# Zabura 45

Don mai bi da kaɗe-kaɗe. Da salon "Lili." Na 'ya'yan Kora maza. *Maskil** Waƙar Aure.

1 Zuciyata ta cika da kyakkyawan kan magana
yayinda nake rera ayoyina wa sarki;
harshena ne alƙalamin ƙwararren marubuci.

2 Kai ne mafi kyau cikin mutane
an kuma shafe leɓunanka da alheri,
da yake Allah ya albarkace ka har abada.

3 Ka ɗaura takobinka a gefenka, ya jarumi;
ka rufe kanka da ɗaukaka da kuma daraja.
4 Cikin darajarka ka hau zuwa nasara
a madadin gaskiya, tawali'u da adalci;
bari hannunka na dama yă nuna ayyukan banmamaki.
5 Bari kibiyoyinka masu tsini su huda zukatan abokan gāban sarki;
bari al'ummai su fāɗi ƙarƙashin ƙafafunka.
6 Kursiyinka, ya Allah, zai kasance har abada abadin;
sandar adalci zai zama sandar mulkinka.
7 Kana ƙaunar abin da yake daidai kana kuma ƙin mugunta;
saboda haka Allah, Allahnka, ya sa ka a bisa abokanka
ta wurin shafe ka da man farin ciki.
8 Dukan rigunanka suna ƙanshin turaren mur da na aloyes, da na kashiya;
daga kowace fadan da aka yi masa ado da hauren giwa
kaɗe-kaɗen tsirkiya kan sa ka murna.
9 'Ya'yan sarki mata suna cikin matan da ake girmama;
a hannun damarka kuwa ga amarya, sarauniya saye da ofir zinariya.

10 Ki saurara, ya ke diya, ki lura ku kuma kasa kunne,
Ki manta da mutanenki da gidan mahaifinki.
11 Sarki ya cika da sha'awar kyanki;
ki girmama shi, gama shi ne maigidanki.
12 Diyar Taya za tă zo da kyauta,
mawadata za su nemi tagomashinki.
13 Gimbiya tana fada, kyakkyawa ce ainun;
an saƙa rigarta da zaren zinariya.
14 Cikin riguna masu ado aka kai ta wurin sarki;
abokanta budurwai suna biye da ita
aka kuwa kawo su gare ka.
15 Aka bi da su cikin farin ciki da murna;
suka shiga fadan sarki.

16 'Ya'yanka maza za su maye matsayin kakanninka;
za ka sa su yi mulki a duk fāɗin ƙasar.

17 Zan sa a tuna da kai a dukan zamanai;
saboda haka al'ummai za su yabe ka har abada abadin.

* **Zabura 45:** Kan magana, mai yiwuwa wata kalmar waƙa ce.

# Zabura 46

Don mai bi da kaɗe-kaɗe. Ta 'Ya'yan Kora maza. Bisa ga *alamot* Waƙa ce.

1 Allah ne mafakarmu da ƙarfinmu,
kullum yana a shirye yă taimaka a lokacin wahala.
2 Saboda haka ba za mu ji tsoro ba, ko da ƙasa ta girgiza
duwatsu kuma suka fāɗi cikin zurfin teku,
3 ko da ruwansa suna ruri suna kumfa
duwatsu kuma suna girgiza da tumbatsansu.

Sela

4 Akwai kogi mai rafuffukan da suke sa birnin Allah murna,
tsattsarkan wuri inda Mafi Ɗaukaka ke zama.
5 Allah yana cikinta, ba za tă fāɗi ba;
Allah zai taimake ta da safe.
6 Al'ummai suna hayaniya, mulkoki sun fāɗi;
ya ɗaga muryarsa, duniya ta narke.

7 UBANGIJI Maɗaukaki yana tare da mu;
Allah na Yaƙub ne kagararmu.

Sela

8 Zo ku ga ayyukan UBANGIJI,
kangon da ya kawo a kan duniya.
9 Ya sa yaƙoƙi suka yi tsit
ko'ina a duniya.
Ya kakkarya bakkuna ya kuma ragargaza māsu,
ya ƙone garkuwoyi* da wuta.
10 "Ku natsu ku kuma san cewa ni ne Allah;
za a ɗaukaka ni a cikin al'ummai,
za a ɗaukaka ni cikin duniya."

11 UBANGIJI Maɗaukaki yana tare da mu;
Allah na Yaƙub ne kagararmu.

Sela

# Zabura 47

Don mai bi da kaɗe-kaɗe. Ta 'Ya'yan Kora maza. Zabura ce.

1 Ku tafa hannuwanku, dukanku al'ummai;
ku yi sowa ga Allah da muryoyin farin ciki.

2 UBANGIJI Mafi Ɗaukaka mai banmamaki ne,
Sarki ne mai girma a bisa dukan duniya!
3 Ya rinjayi al'ummai a ƙarƙashinmu,
mutane kuma a ƙarƙashin ƙafafunmu.
4 Ya zaɓar mana gādonmu,
abar taƙamar Yaƙub, wanda yake ƙauna.

Sela

5 Allah ya haura a cikin sowa ta farin ciki,
UBANGIJI ya haura a cikin ƙarar ƙahoni.
6 Ku rera yabai ga Allah, ku rera yabai;

* **Zabura 46:9** Ko kuwa kekunan yaƙi

ku rera yabai ga Sarkinmu, ku rera yabai.
7 Gama Allah shi ne Sarkin dukan duniya;
ku rera zabura ta yabo gare shi.

8 Allah yana mulki a bisa al'ummai;
Allah yana zama a kan kursiyinsa mai tsarki.
9 Manyan mutanen al'ummai sun taru
a matsayin mutanen Allah na Ibrahim,
gama sarkunan duniya na Allah ne;
ana ɗaukaka shi ƙwarai.

# Zabura 48

Waƙa ce. Zabura ta 'ya'yan Kora maza.
1 UBANGIJI mai girma ne, kuma mafificin yabo,
a birnin Allahnmu, dutsensa mai tsarki.

2 Kyakkyawa ce cikin tsayinta,
abin farin cikin dukan duniya.
Kamar ƙwanƙoli mafi tsayi na Zafon* ne Dutsen Sihiyona,
birnin† Babban Sarki.
3 Allah yana cikin fadodinta;
ya nuna kansa mafaka ce gare ta.

4 Sa'ad da sarakuna suka haɗa rundunoni,
sa'ad da suka yi gaba tare,
5 sun gan ta suka kuwa yi mamaki;
suka gudu don tsoro.
6 Rawar jiki ya kama su a can,
zafi kamar na mace mai naƙuda.
7 Ka hallaka su kamar jiragen ruwan Tarshish
da iskar gabas ta wargaje.

8 Yadda muka ji,
haka muka gani
a cikin birnin UBANGIJI Maɗaukaki,
a cikin birnin Allahnmu.
Allah ya sa ta zauna lafiya
har abada.
Sela

9 Cikin haikalinka, ya Allah,
mun yi tunani a kan ƙaunarka marar ƙarewa.
10 Kamar sunanka, ya Allah,
yabonka ya kai iyakokin duniya;
hannunka na dama ya cika da adalci.
11 Dutsen Sihiyona ya yi farin ciki,
ƙauyukan Yahuda suna murna
saboda hukuntanka.

12 Yi tafiya cikin Sihiyona, ku kewaye ta,

---

* **Zabura 48:2** Zafon yana nufin dutse mai tsarki ko kuwa gefen arewa. † **Zabura 48:2** Ko kuwa duniya, Dutsen Sihiyona, a arewanci na

ku ƙirga hasumiyoyinta,
13 ku lura da katangarta da kyau,
ku dubi fadodinta,
don ku faɗe su
ga tsara mai zuwa.

14 Gama wannan Allah shi ne Allahnmu har abada abadin;
zai zama jagorarmu har zuwa ƙarshe.

# Zabura 49

Don mai bi da kaɗe-kaɗe. Na 'ya'yan Kora maza. Zabura ce.
1 Ku ji wannan, dukanku mutane;
ku saurara, dukanku waɗanda suke zama a wannan duniya,
2 babba da yaro
mai arziki da talaka.
3 Bakina zai yi maganar hikima;
magana daga zuciyata za tă ba da ganewa.
4 Zan juye kunnena ga karin magana;
da garaya zan ƙarfafa kacici-kacicina.

5 Don me zan ji tsoro sa'ad da mugayen kwanaki suka zo,
sa'ad da mugaye masu ruɗu suka kewaye ni,
6 waɗanda suka dogara ga arzikinsu
suna kuma fariya a kan yawan arzikinsu?
7 Ba wani da zai iya ceton ran wani
ko yă ba wa Allah kuɗin fansa saboda shi,
8 kuɗin fansa domin rai yana da tsada,
babu abin da za a biya da ya taɓa isa,
9 da zai sa yă ci gaba da rayuwa har abada
yă hana shi shigan kabari yă ruɓa.
10 Gama kowa na iya ganin masu hikima na mutuwa;
wawaye da marasa azanci su ma kan hallaka
su bar wa waɗansu arzikinsu.
11 Kaburburansu za su ci gaba da zama gidajensu har abada,
Can za su kasance har zamanai marasa ƙarewa,
ko da yake sun ba wa filaye sunayen kansu.

12 Amma mutum, kome arzikinsa, ba ya dawwama;
shi kamar dabbobi ne da suke mutuwa.

13 Wannan ne ƙaddarar waɗanda suke dogara a kansu,
da kuma ta mabiyansu, waɗanda suka tabbatar da faɗinsu.
Sela
14 Kamar tumaki an ƙaddara su ga kabari;
za su kuwa zama abincin mutuwa
amma masu gaskiya za su yi mulki a kansu da safe.
Kamanninsu za su ruɓe a cikin kabari,
nesa da gidajensu masu tsada.
15 Amma Allah zai ceci raina daga kabari;
tabbatacce zai ɗauke ni zuwa wurinsa.
Sela
16 Kada ka razana da yawa sa'ad da mutum ya yi arziki

sa’ad da darajar gidansa ta ƙaru;
17 gama ba zai ɗauki kome tare da shi sa’ad da ya mutu ba,
darajarsa ba za tă gangara tare da shi ba.
18 Ko da yake yayinda yake a raye ya ɗauka kansa mai albarka ne,
mutane kuma sun yabe ka sa’ad da kake cin nasara,
19 zai gamu da tsarar kakanninsa,
waɗanda ba za su taɓa ganin hasken rayuwa ba.

20 Mutumin da yake da arziki ba tare da ganewa ba
shi kamar dabbobi ne da suke mutuwa.

# Zabura 50

Zabura ta Asaf.
1 Maɗaukaki, Allah, UBANGIJI,
ya yi magana ya kuma kira duniya
daga fitowar rana zuwa inda take fāɗuwa.
2 Daga Sihiyona, cikakkiya a kyau,
Allah na haskakawa.
3 Allahnmu yana zuwa
ba kuwa zai yi shiru ba;
wuta mai cinyewa a gabansa,
babban hadari kuma ya kewaye shi.
4 Ya kira sammai da suke bisa,
da duniya, don yă shari’anta mutanensa.
5 “Ku tattara mini shafaffuna,
waɗanda suka yi alkawari da ni ta wurin hadaya.”
6 Sammai kuwa sun yi shelar adalcinsa
gama Allah kansa alƙali ne.

Sela

7 “Ku ji, ya mutanena, zan kuwa yi magana,
Ya Isra’ila, zan kuwa ba da shaida a kanku.
Ni ne Allah, Allahnku.
8 Ba na tsawata muku saboda hadayunku
ko kuwa hadayunku na ƙonawa, waɗanda kuka taɓa kawo a gabana.
9 Ba na bukatan bijimi daga turkenku
ko awaki daga garkunanku,
10 gama kowace dabbar kurmi nawa ne,
da kuma shanu a kan dubban tuddai.
11 Na san kowane tsuntsun da yake a duwatsu
kuma halittun filaye nawa ne.
12 Da a ce ina jin yunwa ai, ba sai na faɗa muku ba,
gama duniyar nawa ne, da kome da yake cikinta.
13 Ina cin naman bijimai ne
ko ina shan jinin awaki ne?

14 “Ku miƙa hadayar godiya ga Allah,
ku cika alkawuranku ga Mafi Ɗaukaka,
15 ku kira gare ni a ranar wahala;
zan cece ku, za ku kuwa girmama ni.”
16 Amma ga mugaye, Allah ya ce,

“Wace dama ce kuke da ita na haddace dokokina
ko na yin maganar alkawarina a leɓunanku?
17 Kun ƙi umarnina
kuka kuma zubar da kalmomina a bayanku
18 Sa’ad da kuka ga ɓarawo, kukan haɗa kai da shi;
kukan haɗa kai da mazinata.
19 Kuna amfani da bakunanku don mugunta
kuna kuma gyara harshenku don ruɗu.
20 Kuna ci gaba da magana a kan ɗan’uwanku
ku kuma yi maganar ƙarya a kan ɗan mahaifinku.
21 Kun yi waɗannan abubuwa na kuwa yi shiru;
kun ɗauka gaba ɗaya ni kamar ku ne.
Amma zan tsawata muku
in kuma zarge ku a fuskarku.

22 “Ku lura da wannan, ku da kuka manta da Allah,
ko kuwa in yayyage ku kucu-kucu, ba kuma wanda zai cece ku.
23 Shi wanda ya miƙa hadayun godiya yakan girmama ni,
ya kuma shirya hanya saboda in nuna masa* ceton Allah.”

# Zabura 51

Don mai bi da kaɗe-kaɗe. Zabura ta Dawuda. Sa’ad da annabi Natan ya zo wurinsa bayan Dawuda ya yi zina da Batsheba.

1 Ka yi mini jinƙai, ya Allah,
bisa ga ƙaunarka marar ƙarewa;
bisa ga tausayinka mai girma
ka shafe laifofina.
2 Ka wanke dukan kurakuraina
ka tsarkake ni daga zunubina.

3 Gama ina sane da laifofina
zunubaina kuma kullum suna a gabana.
4 Kai kaɗai na yi wa zunubi
na yi abin da yake mugu a idonka,
ta haka an tabbatar kai mai gaskiya sa’ad da ka yi magana
aka kuma nuna kai mai adalci ne sa’ad da ka hukunta.
5 Tabbatacce ni mai zunubi ne tun haihuwa
mai zunubi daga lokacin da mahaifiyata ta yi cikina.
6 Tabbatacce kana son gaskiya a sassan ciki;
ka koya mini hikima a wuri can ciki.

7 Ka tsarkake ni da hizzob, zan kuwa zama tsab;
ka wanke ni, zan kuma fi dusan ƙanƙara fari.
8 Bari in ji farin ciki da murna;
bari ƙasusuwan da ka ragargaza su yi farin ciki.
9 Ka ɓoye fuskarka daga zunubaina
ka kuma shafe dukan kurakuraina.

10 Ka halitta zuciya mai tsabta a cikina, ya Allah,
ka kuma sabunta tsayayyen ruhu a cikina.
11 Kada ka fid da ni daga gabanka

* **Zabura 50:23** Ko kuwa gare shi kuma wanda ya lura da hanyarsa / zan nuna

ko ka ɗauke Ruhunka Mai Tsarki daga gare ni.
12 Ka mayar mini farin cikin cetonka
ka kuma ba ni ruhun biyayya, yǎ riƙe ni.

13 Ta haka zan koyar wa masu laifi hanyoyinka,
masu zunubi kuma za su komo gare ka.
14 Ka cece ni daga laifin jini, ya Allah,
Allahn da ya cece ni,
harshena kuwa zai rera adalcinka.
15 Ya Ubangiji, ka buɗe leɓunana,
bakina kuwa zai furta yabonka.
16 Ba ka farin ciki a hadaya, ai da na kawo;
ba ka jin daɗin hadayun ƙonawa.
17 Hadayun Allah su ne karyayyen ruhu;
karyayyiya da kuma zuciya mai tuba,
Ya Allah, ba za ka ƙi ba.

18 Cikin jin daɗinka ka sa Sihiyona ta yi nasara;
ka gina katangar Urushalima.
19 Ta haka za a kasance da hadayu masu adalci,
hadayun ƙonawa ɗungum don su faranta ka;
sa’an nan za a miƙa bijimai a bagadenka.

# Zabura 52

Don mai bi da kaɗe-kaɗe. Wani *maskil** ta Dawuda. Sa’ad da Doyeg mutumin Edom ya tafi wurin Shawulu ya ce masa, “Dawuda ya tafi gidan Ahimelek.”
1 Me ya sa kake fariya game da mugunta, kai babban mutum?
Me ya sa kake fariya dukan yini,
kai da kake abin kunya a idanun Allah?
2 Harshenka kan shirya hallaka;
yana nan kamar reza mai ci,
kana ta ruɗu.
3 Kana ƙaunar mugunta fiye da alheri,
ƙarya a maimakon faɗin gaskiya.

Sela

4 Kana ƙaunar kowace kalmar cutarwa,
Ya kai harshe mai ruɗu!

5 Tabbatacce Allah zai kai ka ga madawwamiyar hallaka.
Zai fizge ka yǎ yayyage ka daga tentinka;
zai tumɓuke ka daga ƙasar masu rai.

Sela

6 Masu adalci za su ga su ji tsoro;
za su yi masa dariya, suna cewa,
7 “Yanzu, ga mutumin
da bai mai da Allah mafakarsa ba
amma ya dogara a yawan arzikinsa
ya kuma yi ƙarfi ta wurin hallaka waɗansu!”

8 Amma ni kamar itace zaitun ne

* **Zabura 52:** Kan magana, mai yiwuwa wata kalmar waƙa ce.

ina haɓaka a gidan Allah;
na dogara ga ƙauna marar ƙarewa ta Allah
har abada abadin.
9 Zan yabe ka har abada game da abin da ka yi;
a cikin sunanka zan dogara, gama sunanka yana da kyau.
Zan yabe ka a gaban tsarkakanka.

# Zabura 53

Don mai bi da kaɗe-kaɗe. Bisa ga *mahalat.*[*] Wani *maskil*[†] na Dawuda.

1 Wawa ne kawai yakan ce a zuciyarsa,
"Ba Allah."
Sun lalace, kuma hanyoyinsu ba su da kyau;
babu wani mai aikata abu mai kyau.

2 Allah yana duba daga sama
a kan 'ya'yan mutane
yă ga ko akwai wani wanda ya gane,
wani wanda yake neman Allah.
3 Kowa ya kauce, gaba ɗaya sun lalace;
babu guda da yake aikata abu mai kyau,
babu ko ɗaya.

4 Masu aikata mugunta ba sa taɓa koyo?

Suna cin mutanena kamar yadda ake cin burodi,
ba sa kuma kira ga Allah.
5 Ga shi fa, sun firgita don tsoro,
ko da yake babu dalilin tsoro,
gama Allah zai watsar da ƙasusuwan masu ƙinsa,
za su sha kunya, gama Allah ya ƙi su.

6 Kash, da ceton Isra'ila zai fito daga Sihiyona mana!
Sa'ad da Allah ya sāke arzuta mutanensa,
bari Yaƙub yă yi farin ciki Isra'ila kuma yă yi murna!

# Zabura 54

Don mai bi da kaɗe-kaɗe. Da kayan kiɗi masu tsirkiya. Wani *maskil*[*] ta Dawuda. Sa'ad da Zifawa suka tafi wurin Shawulu suka ce, "Ba Dawuda ba ne yake ɓuya a cikinmu?"

1 Ka cece ni, ya Allah ta wurin sunanka;
ka nuna ni marar laifi ne ta wurin ƙarfinka.
2 Ka ji addu'ata, ya Allah;
ka saurari maganar bakina.

3 Baƙi suna kawo mini hari;
mutane marasa imani suna neman raina,
mutanen da ba sa tsoron Allah.

Sela

[*] **Zabura 53:** Kan magana, mai yiwuwa wata kalmar waƙa ce. [†] **Zabura 53:** Kan magana, mai yiwuwa wata kalmar waƙa ce. [*] **Zabura 54:** Kan magana, mai yiwuwa kalmar waƙa ce.

4 Tabbatacce Allah ne mai taimakona,
Ubangiji shi ne wanda yake riƙe ni.

5 Bari mugunta ta shaƙe masu magana marar kyau a kaina;
cikin amincinka ka hallaka su.

6 Zan miƙa hadaya ta yardar rai gare ka;
zan yabe sunanka, ya UBANGIJI, gama yana da kyau.
7 Gama ya cece ni daga dukan wahalolina,
idanuna kuma sun ga an yi nasara a kan maƙiyana.

# Zabura 55

Don mai bi da kaɗe-kaɗe. Da kayan kiɗi masu tsirkiya. Wani *maskil** ta Dawuda.
1 Ka ji addu'ata, ya Allah,
kada ka ƙyale roƙona;
2 ka ji ni ka kuma amsa mini.
Tunanina yana damuna na kuma gaji tilis
3 hankalina ya tashi saboda yawan surutan masu ƙina,
saboda danniyar mugaye.
Gama sukan jawo mini wahala,
suna jin haushina suna ƙina.

4 Zuciyata tana wahala a cikina;
tsorace-tsoracen mutuwa sun sha kaina.
5 Tsoro da rawan jiki sun kama ni;
razana ta sha kaina.
6 Na ce, "Kash, da a ce ina da fikafikan kurciya mana!
Ai, da na yi firiya na tafi na huta,
7 da na tafi can da nisa
na zauna a hamada;
Sela
8 da na hanzarta na tafi wurin mafakata,
nesa da muguwar iska da hadiri."

9 Ka rikitar da mugaye, ya Ubangiji, ka birkitar da maganarsu,
gama na ga rikici da faɗa a cikin birni.
10 Dare da rana suna yawo a kan katanga;
mugun hali da zargi suna a cikinta.
11 Rundunar hallaka suna aiki a cikin birni;
barazana da ƙarairayi ba sa taɓa barin titunanta.

12 Da a ce abokin gāba ne ke zagina,
da na jure da shi;
da a ce maƙiyi yana tā da kansa a kaina,
da na ɓoye daga gare shi.
13 Amma kai ne, mutum kamar ni,
abokina, abokina na kurkusa,
14 wanda na taɓa jin daɗin zumunci da shi sosai
yayinda muke tafiya tare
a taron jama'a a gidan Allah.

---

* **Zabura 55:** Kan magana, mai yiwuwa wata kalmar waƙa ce.

15 Bari mutuwa ta ɗauki abokan gābana ba labari;
bari su gangara da rai zuwa cikin kabari,
gama mugunta tana samun masauƙi a cikinsu.

16 Amma na kira ga Allah,
UBANGIJI kuwa ya cece ni.
17 Safe, rana da yamma
ina kuka da nishi,
yakan kuwa ji muryata.
18 Yakan fisshe ni lafiya
daga yaƙin da ake yi da ni,
ko da yake da yawa suna gāba da ni.
19 Allah, yana mulki har abada,
zai ji su yă kuma azabtar da su,
Sela
mutanen da ba sa taɓa canja hanyoyinsu
kuma ba sa tsoron Allah.

20 Abokina ya kai wa abokansa hari;
ya tā da alkawarinsa.
21 Maganarsa tana da laushi kamar man zaitun,
duk da haka yaƙi yana a cikin zuciyarsa;
kalmominsa sun fi mai sulɓi,
duk da haka takuba ne zārarru.

22 Ku kawo damuwoyinku ga UBANGIJI
zai kuwa riƙe ku;
ba zai taɓa barin
mai adalci yă fāɗi ba.
23 Amma kai, ya Allah, za ka kawar da mugaye
zuwa cikin ramin lalacewa;
masu kisa da mutane masu ruɗu
ba za su kai rabin kwanakin rayuwarsu ba.

Amma ni dai, na dogara gare ka.

# Zabura 56

Don mai bi da kaɗe-kaɗe. Da murya “Kurciya a Itatuwan Oak Mai Nisa.” Ta Dawuda. Wani *miktam.** Sa’ad da Filistiyawa suka kama shi a birnin Gat.
1 Ka yi mini jinƙai,
ya Allah, gama mutane sun tasar mini da zafi;
dukan yini suna matsa harinsu.
2 Masu ɓata sunana suna bina dukan yini;
da yawa suna kai mini hari cikin fariyarsu.

3 Sa’ad da nake tsoro, zan dogara gare ka.
4 Ga Allah wanda maganarsa nake yabo
ga Allah na dogara; ba zan ji tsoro ba.
Me mutum mai mutuwa zai yi mini?

* **Zabura 56:** Kan magana, mai yiwuwa wata kalmar waƙa ce.

5 Dukan yini sun yi ta juya maganata;
kullum suna ƙulle-ƙulle su cuce ni.
6 Sun haɗa baki, sun ɓoye,
suna kallon takawata
suna a shirye su ɗauki raina.
7 Sam, kada ka bari su kuɓuce;
cikin fushinka, ya Allah, ka saukar da al'ummai.

8 Ka lissafta makokina;
ka jera hawayena a littafinka,†
ba a rubuce suke a cikin littafinka ba?
9 Ta haka abokan gābana za su juya da baya
sa'ad da na nemi taimako.
Ta haka zan san cewa Allah yana tare da ni.

10 Ga Allah, wanda nake yabon maganarsa,
ga UBANGIJI, wanda nake yabon maganarsa,
11 ga Allah na dogara; ba zan ji tsoro ba.
Me mutum zai iya yi mini?

12 Ina ƙarƙashin alkawari gare ka, ya Allah;
zan miƙa hadayuna na godiya gare ka.
13 Gama ka cece ni‡ daga mutuwa
da kuma ƙafafun daga tuntuɓe,
don in yi tafiya a gaban Allah
cikin hasken rai.§

# Zabura 57

Don mai bi da kaɗe-kaɗe. Da muryar "Kada Ka Hallaka." Ta Dawuda. Wani *miktam.**
Sa'ad da ya gudu daga Shawulu zuwa cikin kogo.
1 Ka yi mini jinƙai, ya Allah, ka yi mini jinƙai,
gama a gare ka raina yake samun mafaka.
Zan sami mafaka a inuwar fikafikanka
sai masifar ta wuce.

2 Na yi kuka ga Allah Mafi Ɗaukaka,
ga Allah, wanda yake cika manufarsa gare ni.
3 Ya aika daga sama ya kuwa cece ni,
yana tsawata wa waɗanda suke fafarata da zafi;
Sela
Allah yakan aika da ƙaunarsa da amincinsa.

4 Ina tsakiyar zakoki;
ina kwance a cikin namun jeji masu cin mutane,
mutanen da haƙoransu masu ne da kuma kibiyoyi,
waɗanda harshensu suna da kaifi kamar takobi.

5 Bari a ɗaukaka ka, ya Allah, bisa sammai;
bari ɗaukakarka ta kasance a dukan duniya.

---

† **Zabura 56:8** Ko kuwa / ka sa hawayena a salkan ruwan inabinka ‡ **Zabura 56:13** Ko kuwa raina § **Zabura 56:13** Ko kuwa a ƙasar masu rai * **Zabura 57:** Kan magana, mai yiwuwa wata kalmar waƙa ce.

6 Sun shimfiɗa raga don su kama ƙafafuna,
damuwa ta sha ƙarfina.
Sun haƙa rami a hanyata,
amma su kansu suka fāɗa a cikinta.
Sela

7 Zuciyata tana nan daram, ya Allah,
zuciyata tana nan daram;
zan rera in kuma yi kaɗe-kaɗe.
8 Ka farka, raina!
Ku farka, garaya da molo!
Zan sa safe yă farka.

9 Zan yabe ka, ya Ubangiji, a cikin al'ummai;
zan rera game da kai a cikin mutane.
10 Gama ƙaunarka mai girma ce, tana kaiwa sammai;
amincinka na kaiwa sarari.

11 Bari a ɗaukaka ka, ya Allah, bisa sammai;
bari ɗaukakarka ta kasance a dukan duniya.

# Zabura 58

Don mai bi da kaɗe-kaɗe. Da muryar "Kada Ka Hallaka." Ta Dawuda. Wani *miktam*.*
1 Ku masu mulki tabbatacce kuna magana daidai?
Kuna yin shari'a daidai a cikin mutane?
2 Sam, a zuciyarku kuna ƙirƙiro rashin adalci,
da hannuwanku kuma kuna tā da hargitsi a duniya.

3 Kai, tun haihuwa mugaye sukan kauce;
daga cikin ciki, su lalatattu ne maƙaryata.
4 Dafinsu ya yi kamar dafin maciji,
kamar na gamsheƙan da ya toshe kunnuwansa,
5 da ba ya jin muryar gardi,
kome dabarar gwanin mai waƙar zai zama.

6 Ka kakkarya haƙoran a bakunansu, ya Allah;
ka yayyage fiƙoƙin zakoki, ya Ubangiji!
7 Bari su ɓace kamar ruwa mai wucewa;
sa'ad da suka ja bakansu, bari kibiyoyinsu su murtsuke.
8 Kamar katantanwun da suke narkewa yayinda suke tafiya,
kamar jinjirin da aka haifa matacce, kada su ga hasken rana.

9 Kafin tukwanenka su ji zafin ƙayayyuwa,
ko su kore ne ko busasshe, za a shafe mugaye.†
10 Masu adalci za su yi murna sa'ad da aka rama musu,
sa'ad da suka wanke ƙafafunsu cikin jinin mugaye.
11 Sa'an nan mutane za su ce,
"Tabbatacce har yanzu ana sāka wa adalai;
tabbatacce akwai Allahn da yake shari'anta duniya."

* **Zabura 58:** Kan magana, mai yiwuwa wata kalmar waƙa ce. † **Zabura 58:9** Ma'anar Ibraniyancin wannan aya ba tabbatacce ba ne.

# Zabura 59

Don mai bi da kaɗe-kaɗe. Da muryar “Kada Ka Hallaka.” Ta Dawuda. Wani *miktam.**
Sa’ad da Shawulu ya aiki mutane su yi tsaron gidan Dawuda don yă kashe shi.
1 Ka cece ni daga abokan gābana, ya Allah;
ka tsare ni daga waɗanda suka tayar mini.
2 Ka kuɓutar da ni daga masu aikata mugunta
ka kuma cece ni daga masu kisa.

3 Duba yadda suka kwanta suna jirana!
Mugaye suna ƙulle-ƙullen gāba da ni
ba saboda wani dalili ko na yi wa wani zunubi ba, ya Ubangiji.
4 Ban yi wani laifi ba, duk da haka suna a shirye su fāɗa mini.
Tashi ka taimake ni; dubi halin da nake ciki!
5 Ya Ubangiji Allah Maɗaukaki,
Allah na Isra’ila,
ka tashi ka hukunta dukan al’ummai;
kada ka nuna jinƙai ga mugaye maciya amana.
Sela

6 Sukan dawo da yamma,
suna wage haƙora kamar karnuka,
suna yawo a birni.
7 Dubi abin da suke tofawa daga bakunansu,
suna tofar da takuba daga leɓunansu,
suna cewa, “Wa zai ji mu?”
8 Amma kai, ya Ubangiji, kakan yi musu dariya;
kana yi wa dukan waɗannan al’ummai ba’a.

9 Ya ƙarfina, na dogara gare ka;
kai, ya Allah, kai ne kagarata, 10 Allah mai ƙaunata.

Allah zai sha gabana
zai kuma sa in yi dariya a kan waɗanda suke magana marar kyau a kaina.
11 Amma kada ka kashe su, ya Ubangiji garkuwarmu,
in ba haka mutanena za su manta.
Cikin ikonka ka sa su yi ta yawo barkatai,
ka kuma kawar da su.
12 Saboda zunuban bakunansu,
saboda maganganun leɓunansu,
bari a kama su cikin fariyarsu.
Saboda zage-zage da ƙarairayin da suke yi,
13 ka cinye su da hasala,
ka cinye su sarai.
Sa’an nan za a sani a iyakar duniya
cewa Allah yana mulki a bisa Yaƙub.
Sela

14 Sukan dawo da yamma,
suna wage haƙora kamar karnuka,
suna yawo a birni.

* **Zabura 59:** Kan magana, mai yiwuwa wata kalmar waƙa ce.

15 Suna ta yawo neman abinci
su kuwa yi haushi in ba su ƙoshi ba.
16 Amma zan rera game da ƙarfinka,
da safe zan rera game da ƙaunarka;
gama kai ne mafakata,
kagarata a lokacin wahala.

17 Ya ƙarfina, na rera yabo gare ka;
kai, ya Allah, kai ne kagarata,
Allah mai ƙaunata.

# Zabura 60

Don mai bi da kaɗe-kaɗe. Da muryar "Lilin Alkawari." Wani *miktam*[*] ta Dawuda. Don koyarwa. Sa'ad da ya yaƙi Aram-Naharayim[†] da Aram-Zoba,[‡] da kuma sa'ad da Yowab ya dawo ya bugi mutanen Edom dubu goma sha biyu a Kwarin Gishiri.
1 Ka ki mu, ya Allah, ka kuma fashe kāriyarmu;
ka yi fushi da mu, yanzu ka mai da mu!
2 Ka girgiza ƙasar ka kuma tsaga ta;
ka daure karayarta, gama tana rawa.
3 Ka nuna wa mutanenka lokutan wahala;
ka ba mu ruwan inabin da ya sa muka bugu.
4 Amma ga waɗanda suke tsoronka, ka ɗaga tuta
don a buɗe gāba da baka.

Sela

5 Ka cece mu ka kuma taimake mu da hannunka na dama,
domin waɗanda kake ƙauna su kuɓuta.
6 Allah ya yi magana daga wurinsa mai tsarki,
"Da nasara zan rarraba Shekem
in kuma auna Kwarin Sukkot.
7 Gileyad nawa ne, Manasse kuma nawa ne;
Efraim shi ne hular kwanona,
Yahuda kuma sandar mulkina.
8 Mowab shi ne kwanon wankina,
a kan Edom zan jefa takalmina;
a bisa Filistiya zan yi kirarin nasara."

9 Wa zai kawo ni birnin katanga?
Wa zai bishe ni zuwa Edom?
10 Ba kai ba ne, ya Allah, kai da ka ƙi mu
ba ka kuwa fita tare da mayaƙanmu?
11 Ka ba mu gudummawa a kan abokin gāba,
gama taimakon mutum banza ne.
12 Tare da Allah za mu yi nasara,
zai kuma tattake abokan gābanmu.

# Zabura 61

Don mai bi da kaɗe-kaɗe. Da kayan kiɗi masu tsirkiya. Ta Dawuda.
1 Ka ji kukata, ya Allah;

---

[*] **Zabura 60:** Kan magana, mai yiwuwa wata kalmar waƙa ce. [†] **Zabura 60:** Kan Magana. Wato, Arameyawan Arewa maso Yamma na Mesofotamiya. [‡] **Zabura 60:** Kan magana, wato, Arameyawan Tsakiyar Suriya.

ka saurari addu'ata.

2 Daga iyakar duniya na yi kira gare ka,
na yi kira yayinda zuciyata ta karai;
ka bishe ni zuwa dutsen da ya fi ni tsayi.
3 Gama kai ne mafakata,
hasumiya mai ƙarfi gāba da maƙiyi.

4 Ina marmari in zauna a tentinka har abada
in sami mafaka a cikin inuwar fikafikanka.
Sela
5 Gama ka ji alkawarina, ya Allah;
ka ba ni gādo na waɗanda suke tsoron sunanka.

6 Ka ƙara kwanakin ran sarki,
shekarunsa su kasance a zamanai masu yawa.
7 Bari yă yi mulki a gaban Allah har abada;
ka sa ƙaunarka da amincinka su tsare shi.

8 Sa'an nan zan riƙa rera yabo ga sunanka
in kuma cika alkawarina kowace rana.

# Zabura 62

Don mai bi da kaɗe-kaɗe. Don Yedutun. Zaburar Dawuda.
1 Raina na samun hutu a wurin Allah ne kaɗai;
cetona na zuwa daga gare shi.
2 Shi kaɗai ne dutsena da cetona;
shi ne kagarata, ba zan jijjigu ba.

3 Har yaushe za ku tasar wa mutum guda?
Dukanku ne za ku kā da shi
wannan jingananen bango, wannan rusasshen katanga?
4 Sun kintsa sosai su tumɓuke shi
daga matsayinsa mai martaba;
suna jin daɗi yin ƙarairayi.
Sukan sa wa mutum albarka da bakinsu,
amma a zuciyarsu la'antawa suke yi.
Sela

5 Ka nemi hutu, ya raina, a wurin Allah kaɗai;
dogarata kan zo daga gare shi ne.
6 Shi ne kaɗai dutsena da cetona;
shi ne kagarata, ba zan jijjigu ba.
7 Cetona da girmata sun dangana ga Allah ne,*
shi ne dutsena mai ƙarfi, mafakata.
8 Ku dogara a gare shi a duk lokuta, ya mutane;
ku faɗi albarkaci bakin zukatanku a gare shi,
gama Allah ne mafakarmu.
Sela

9 Talakawa dai kamar shaƙar iska suke,
Attajirai dai kamar shirim suke;

* **Zabura 62:7** Ko kuwa / Allah Mafi Ɗaukaka shi ne cetona da girmata

in aka auna a ma'auni, su ba wani abu ba ne;
dukansu dai kamar shaƙar iska ne kawai.
10 Kada ku dogara a kan ƙwace
ko yin fariya a kayan sata;
ko arzikinku ya ƙaru,
kada ku sa zuciyarku a kansu.

11 Abu guda Allah ya ce,
abubuwa biyu na ji,
"Cewa kai, ya Allah, kake mai ƙarfi,
12 kuma cewa kai, ya Ubangiji, mai ƙauna ne.
Tabbatacce za ka sāka wa kowane mutum
bisa ga abin da ya yi."

# Zabura 63

Zabura ta Dawuda. Sa'ad da yake a hamadar Yahuda.
1 Ya Allah, kai ne Allahna,
da nacewa na neme ka;
raina yana ƙishinka,
jikina yana marmarinka,
cikin busasshiyar ƙasar da ta zozaye
inda babu ruwa.

2 Na gan ka a wuri mai tsarki
na kuma dubi ikonka da ɗaukakarka.
3 Domin ƙaunarka ta fi rai kyau,
leɓunana za su ɗaukaka ka.
4 Zan yabe ka muddin raina,
kuma a cikin sunanka zai ɗaga hannuwana.
5 Raina zai ƙoshi kamar da abinci mafi kyau;
da leɓunan rerawa bakina zai yabe ka.

6 A gadona na tuna da kai;
ina tunaninka dukan dare.
7 Domin kai ne mai taimakona,
ina rera a cikin inuwar fikafikanka.
8 Raina ya manne maka;
hannunka na dama yana riƙe da ni.

9 Su da suke neman raina za su hallaka;
za su gangara zuwa zurfafan duniya.
10 Za a bayar da su ga takobi
su kuma zama abincin karnukan jeji.

11 Amma sarki zai yi farin ciki ga Allah;
dukan waɗanda suke rantse da sunan Allah za su yabe shi,
amma za a rufe bakunan maƙaryata.

# Zabura 64

Don mai bi da kaɗe-kaɗe. Zabura ta Dawuda.
1 Ka ji ni, ya Allah, yayinda nake faɗin abin da yake damuna;
ka tsare raina daga barazanan abokin gāba.

2 Ka ɓoye ni daga ƙulle-ƙullen mugaye,
daga daure dauren wannan taro masu aikata mugunta.
3 Sukan wāsa harsunansu kamar takuba
su harba kalmominsu kamar kibiyoyi masu kisa.
4 Sukan yin kwanto su harbi marar laifi;
sukan yi harbi nan da nan, ba tsoro.

5 Sukan ƙarfafa juna a mugayen ƙulle-ƙullensu,
sukan yi magana yadda za su ɓoye tarkunansu;
su ce, “Wa zai gan su?”*
6 Sukan yi ƙulle-ƙullen rashin adalci su ce,
“Mun gama ƙulla cikakkiyar maƙarƙashiya tsab!”
Zuciyar mutum da tunaninsa, suna da wuyar ganewa.

7 Amma Allah zai harbe su da kibiyoyi;
nan da nan za a buge su su fāɗi.
8 Zai juya harshensu a kansu
yă kuma kawo su ga hallaka;
duk waɗanda suka gan su za su kaɗa kai, suna musu ba’a.
9 Dukan mutane za su ji tsoro;
za su yi shelar ayyukan Allah
su kuma yi tunanin abin da ya aikata.

10 Bari masu adalci su yi farin ciki a cikin UBANGIJI
su kuma nemi mafaka a gare shi;
bari dukan masu gaskiya a zuciya su yabe shi!

# Zabura 65

Don mai bi da kaɗe-kaɗe. Zabura ta Dawuda. Wata waƙa.
1 Yabo ya dace* da kai, ya Allah, a Sihiyona;
a gare ka za mu cika alkawuranmu
2 Ya kai wanda yake jin addu’a
a gare ka dukan mutane za su zo.
3 Sa’ad da zunubai suka sha ƙarfinmu,
ka gafarta† laifofinmu.
4 Masu albarka ne waɗanda ka zaɓa
ka kawo kusa don su zauna a filayenka!
Mun cika da abubuwa masu kyau na gidanka,
na haikalinka mai tsarki.

5 Ka amsa mana da ayyuka masu banmamaki na adalci,
Ya Allah Mai Cetonmu,
begen dukan iyakar duniya
da kuma na tekuna masu nesa,
6 wanda ya yi duwatsu ta wurin ikonka,
bayan ka kintsa kanka da ƙarfi,
7 wanda ya kwantar da rurin tekuna,
rurin raƙumansu,
da kuma tumbatsar al’ummai.

---

* **Zabura 64:5** Ko kuwa mu * **Zabura 65:1** Ko kuwa kan jira; ma’anar Ibraniyanci na wannan kalma ba a tabbatar ba. † **Zabura 65:3** Ko kuwa ka yi kafara domin

8 Waɗanda suke zama can da nesa sukan ji tsoron manyan ayyukanka;
inda safe ke haskaka yamma kuma ta shuɗe
kakan sa a yi waƙoƙin farin ciki.

9 Kana kula da ƙasa kana kuma yi mata banruwa;
kana azurta ta a yalwace.
Rafuffukan Allah sun cika da ruwa
don su ba mutane hatsi,
don haka ne ka ƙaddara.‡
10 Ka kwarara ta da ruwa ka kuma baje kunyoyinta;
ka sa ta yi laushi da yayyafi ka kuma albarkaci tsire-tsirenta.
11 Saboda alherinka, ya Allah, an sami kaka mai albarka,
amalankenka kuwa sun cika har suna zuba.
12 Makiyayan hamada sun cika har suna zuba;
tuddai sun rufu da murna.
13 Wurin dausayin kiwo sun rufu da garkuna
kwari kuma sun cika da hatsi;
suna sowa don farin ciki.

# Zabura 66

Don mai bi da kaɗe-kaɗe. Zabura ta Dawuda. Waƙa. Zabura.
1 Ku yi sowa ta farin ciki ga Allah, dukan duniya!
2 Ku rera ɗaukaka ga sunansa;
ku sa yabonsa yă zama da ɗaukaka!
3 Ku ce wa Allah, "Ayyukanka da banmamaki suke!
Ikonka da girma yake
har abokan gābanka suna durƙusa a gabanka.
4 Dukan duniya sun rusuna a gabanka
suna rera yabo gare ka,
suna rera yabo ga sunanka."

Sela

5 Ku zo ku ga abin da Allah ya yi,
ayyukansa masu banmamaki a madadin mutum!
6 Ya juya teku zuwa busasshiyar ƙasa,
sun wuce cikin ruwaye da ƙafa,
ku zo, mu yi farin ciki a cikinsa.
7 Yana mulki har abada ta wurin ikonsa,
idanunsa suna duban al'ummai,
kada 'yan tawaye su tayar masa.

Sela

8 Ku yabi Allahnku, ya mutane,
bari a ji ƙarar yabonsa;
9 ya adana rayukanmu
ya kuma kiyaye ƙafafunmu daga santsi.
10 Gama kai, ya Allah, ka gwada mu;
ka tace mu kamar azurfa.
11 Ka kawo mu cikin kurkuku
ka kuma jibga kaya masu nauyi a bayanmu.
12 Ka bar mutane suka hau a kawunanmu;

‡ **Zabura 65:9** Ko kuwa don haka ne ka shirya ƙasar

mun bi ta wuta da ruwa,
amma ka kawo mu zuwa wurin yalwa.

13 Zan zo haikalinka da hadayun ƙonawa
zan kuwa cika alkawurana gare ka,
14 alkawuran da leɓunana suka yi alkawari bakina kuma ya faɗa
sa'ad da nake cikin wahala.
15 Zan miƙa kitsen dabbobi gare ka
da kuma baye-baye na raguna;
zan miƙa bijimai da awaki.
Sela

16 Ku zo ku saurara, dukanku waɗanda suke tsoron Allah;
bari in faɗa muku abin da ya yi mini.
17 Na yi kuka gare shi da bakina;
yabonsa yana a harshena.
18 Da a ce na ji daɗin zunubi a zuciyata,
da Ubangiji ba zai saurara ba;
19 amma tabbatacce Allah ya saurara
ya kuma ji muryata a cikin addu'a.
20 Yabo ga Allah,
wanda bai ƙi addu'ata ba
ko yă janye ƙaunarsa daga gare ni!

# Zabura 67

Don mai bi da kaɗe-kaɗe. Tare da kayan kiɗi masu tsirkiya. Zabura. Waƙa.
1 Bari Allah yă yi mana alheri yă kuma albarkace mu
yă kuma sa fuskarsa ta haskaka a kanmu,
Sela
2 don a san hanyoyinka a duniya,
cetonka kuma a cikin dukan al'ummai.

3 Bari mutane su yabe ka, ya Allah;
bari dukan mutane su yabe ka.
4 Bari al'ummai su yi murna su kuma rera don farin ciki,
gama kana mulkin mutanenka da adalci
kana kuma bi da al'umman duniya.
Sela
5 Bari mutane su yabe ka, ya Allah;
bari dukan mutane su yabe.

6 Sa'an nan ƙasa za tă ba da girbinta
Allah kuma, Allahnmu, zai albarkace mu.
7 Allah yă sa mana albarka,
dukan iyakar duniya kuma su ji tsoronsa.

# Zabura 68

Don mai bi da kaɗe-kaɗe. Ta Dawuda. Zabura. Waƙa.
1 Bari Allah yă tashi, bari a watsar da abokan gābansa;
bari maƙiyansa su gudu a gabansa.
2 Kamar yadda iska take hura hayaƙi, bari yă hura su haka;
kamar yadda kaki kan narke a gaban wuta,

bari mugaye su hallaka a gaban Allah.
3 Amma bari adalai su yi murna
su kuma yi farin ciki a gaban Allah;
bari su yi murna da farin ciki.

4 Rera wa Allah, rera yabo ga sunansa,
ku ɗaukaka wanda yake hawa a kan gizagizai;*
sunansa UBANGIJI ne, ku kuma yi farin ciki a gabansa.
5 Uba ga marayu, mai kāre gwauraye,
shi ne Allah a mazauninsa mai tsarki.
6 Allah ya shirya masu kaɗaici a cikin iyalai,
ya jagorance 'yan kurkuku da waƙoƙi;
amma 'yan tawaye suna zama a ƙasa mai zafin rana.

7 Sa'ad da ka fito a gaban mutanenka, ya Allah,
sa'ad da ka taka ta cikin ƙasar da take wofi,
Sela
8 duniya ta girgiza, sammai suka zuba ruwan sama,
a gaban Allah, wanda ya bayyana a Sinai,
a gaban Allah, Allah na Isra'ila.
9 Ka ba da yayyafi a yalwace, ya Allah;
ka rayar da gādonka da ya gāji.
10 Mutanenka suka zauna a cikinsa,
kuma daga yalwarka, ya Allah, ka tanada wa matalauta.

11 Ubangiji ya yi umarni,
mutane masu yawa ne suka yi shelarsa,
12 "Sarakuna da mayaƙa suka gudu a gaggauce;
cikin sansani mutane sun raba ganima.
13 Har yayinda kuke barci a cikin garken tumaki,
an dalaye fikafikan kurciya da azurfa,
fikafikanta da zinariya mai ƙyalli."
14 Sa'ad da Maɗaukaki ya watsar da sarakuna a cikin ƙasa,
sai ya zama kamar ƙanƙara ta sauka a kan Zalmon.

15 Duwatsun Bashan, duwatsu masu alfarma ne;
duwatsun Bashan masu wuyar hawa ne.
16 Don me kuke duba da kishi, ya duwatsu masu wuyan hawa,
a kan dutsen da Allah ya zaɓa yă yi mulki,
inda UBANGIJI kansa zai zauna har abada?
17 Karusan Allah ninkin dubbai goma ne
da kuma dubu dubbai;
Ubangiji ya zo daga Sinai ya shiga cikin haikalinsa.
18 Sa'ad da ka hau bisa,
ka bi da kamammu cikin tawagarka;
ka karɓi kyautai daga mutane,
har ma daga 'yan tawaye,
don kai, ya UBANGIJI Allah, za ka zauna a can.

* **Zabura 68:4** Ko kuwa / ku shirya hanya wa shi da yake hawan ta hamada

19 Yabo ya tabbata ga Ubangiji, ga Allah Mai Cetonmu,
wanda kullum yake ɗaukan nauyinmu.
Sela
20 Allahnmu shi ne Allah wanda yake ceto;
daga Ubangiji Mai Iko Duka kuɓuta yake zuwa daga mutuwa.
21 Tabbatacce Allah zai murƙushe kawunan abokan gābansa,
rawanin gashi na waɗanda suke ci gaba cikin zunubansa.
22 Ubangiji ya ce, "Zan kawo su daga Bashan;
zan kawo su daga zurfafan teku,
23 don ku wanke ƙafafunku a cikin jinin maƙiyanku,
yayinda harsunan karnukanku su sami rabonsu."

24 Jerin gwanonka ya zo a bayyane, ya Allah,
jerin gwanon Allahna da Sarkina zuwa cikin wuri mai tsarki.
25 A gaba akwai mawaƙa, a bayansu akwai makaɗa;
tare da su akwai 'yan mata suna bugan ganguna.
26 Ku yabi Allah cikin taro mai girma;
yabi Ubangiji cikin taron Isra'ila.
27 Ga ƙaramar kabilar Benyamin, suna jagorance su,
ga babbar ƙungiya shugabannin Yahuda,
ga kuma shugabannin Zebulun da na Naftali.

28 Ka bayyana ikonka, ya Allah;
ka nuna ƙarfinka, ya Allah, kamar yadda ka yi a dā.
29 Saboda haikalinka a Urushalima
sarakuna za su kawo maka kyautai.
30 Ka tsawata wa naman jejin nan a cikin kyauro,
garken bijimai a cikin 'yan maruƙan al'ummai.
Ka ƙasƙantar, bari yă kawo sandunan azurfa.
Ka watsar da al'ummai waɗanda suke jin daɗin yaƙi.
31 Jakadu za su zo daga Masar;
Kush za tă miƙa kanta ga Allah.

32 Ku rera wa Allah, ya masarautan duniya,
ku rera yabo ga Ubangiji,
Sela
33 gare shi wanda yake hawan daɗaɗɗen sararin sama,
wanda yake tsawa da babbar murya.
34 Ku yi shelar ikon Allah,
wanda ɗaukakarsa take a bisa Isra'ila,
wanda ikonsa yake a cikin sarari.
35 Kai mai banmamaki ne, ya Allah, cikin wurinka mai tsarki;
Allah na Isra'ila yakan ba da iko da kuma ƙarfi ga mutanensa.

Yabo ya tabbata ga Allah!

# Zabura 69

Don mai bi da kaɗe-kaɗe. Da muryar "Lilin." Ta Dawuda.
1 Ka cece ni, ya Allah,
gama ruwa ya kai wuyata
2 Na nutse cikin laka mai zurfi,

inda babu wurin tsayawa.
Na shiga cikin ruwaye masu zurfi;
rigyawa ya sha kaina.
3 Na gaji da kira ina neman taimako;
maƙogwarona ya bushe
idanuna sun dushe,
suna neman Allahna.
4 Waɗanda suke ƙina ba dalili
sun fi gashin kaina yawa;
da yawa ne abokan gābana babu dalili,
su da suke nema su hallaka ni.
An tilasta mini in
mayar da abin da ban sata ba.

5 Ka san wautata, ya Allah;
laifina ba a ɓoye yake daga gare ka ba.

6 Bari waɗanda suke sa zuciya gare ka
kada su sha kunya saboda ni,
Ya Ubangiji, UBANGIJI Maɗaukaki;
bari waɗanda suke neman ka
kada su sha kunya saboda ni,
Ya Allah na Isra'ila.
7 Gama na jimre da ba'a saboda kai,
kunya kuma ta rufe fuskata.
8 Ni baƙo ne a cikin 'yan'uwana,
bare kuma ga 'ya'yan mahaifiyata maza;
9 gama himma da nake yi wa gidanka yana ƙunata,
kuma zagi na masu zaginka yana fāɗuwa a kaina.
10 Sa'ad da na yi kuka na kuma yi azumi
dole in jimre da ba'a;
11 sa'ad da na sanya rigunan makoki,
mutane suna maishe ni abin dariya.
12 Masu zama a ƙofa suna mini ba'a,
na zama waƙa a bakin bugaggu da giya.

13 Amma na yi addu'a gare ka, ya UBANGIJI,
a lokacin da ka ga dama;
a cikin ƙaunarka mai girma, ya Allah,
ka amsa mini da tabbacin ceto.
14 Ka fid da ni daga laka,
kada ka bari in nutse;
ka cece ni daga waɗanda suke ƙina,
daga rurin ruwaye.
15 Kada ka bar rigyawa yǎ sha kaina
ko zurfafa su haɗiye ni
ko rami yǎ rufe bakinsa a kaina.

16 Ka amsa mini, ya UBANGIJI cikin alherin ƙaunarka;
cikin jinƙanka mai girma ka juyo gare ni.
17 Kada ka ɓoye fuskarka daga bawanka;
ka amsa mini da sauri, gama ina cikin wahala.

18 Ka zo kusa ka kuɓutar da ni;
ka fanshe ni saboda maƙiyana.

19 Ka san yadda ake mini ba'a, ake kunyatar da ni da kuma yadda nake shan kunya;
dukan abokan gābana suna a gabanka.
20 Ba'a ta sa zuciyata ta karai
ta bar ni ba mataimaki;
Na nemi a ji tausayina, amma ban sami ko ɗaya ba,
na nemi masu ta'aziyya, amma ban sami ko ɗaya ba.
21 Sun sa abin ɗaci cikin abincina
suka kuma ba ni ruwan inabi mai tsami sa'ad da nake jin ƙishi.

22 Bari teburin da aka shirya a gabansu yă zama musu tarko;
bari yă zama sakamakon laifi da kuma* tarko.
23 Bari idanunsu yă dushe don kada su gani,
bayansu kuma yă tanƙware har abada.
24 Ka kwarara fushinka a kansu;
bari fushinka mai zafi yă ci musu.
25 Bari wurinsu yă zama kufai;
kada ka bar wani yă zauna a tentunansu.
26 Gama sun tsananta wa waɗanda ka hukunta
suna kuma taɗin wahalar waɗanda ka ji musu rauni.
27 Ka neme su da laifi a kan laifi;
kada ka bar su su sami rabo a cikin cetonka.
28 Bari a shafe su sarai daga littafin rai
kada a kuma lissafta su tare da adalai.

29 Ina cikin zafi da kuma azaba;
bari cetonka, ya Allah, yă tsare ni.

30 Zan yabe sunan Allah cikin waƙa
in kuma ɗaukaka shi tare wurin yin godiya.
31 Wannan zai gamshi UBANGIJI fiye da saniya,
fiye da bijimi da ƙahoninsa da kuma kofatansa.
32 Matalauta za su gani su kuma yi murna,
ku da kuke neman Allah, bari zukatanku su rayu!
33 UBANGIJI yakan ji masu bukata
ba ya kuwa ƙyale kamammun mutanensa.

34 Bari sama da ƙasa su yabe shi,
tekuna da dukan abin da yake motsi a cikinsu,
35 gama Allah zai cece Sihiyona
yă sāke gina biranen Yahuda.
Sa'an nan mutane za su zauna a can su mallake ta,
36 'ya'yan bayinsa za su gāje ta,
waɗanda kuma suna ƙaunar sunansa za su zauna a can.

# Zabura 70

Don mai bi da kaɗe-kaɗe. Ta Dawuda. Roƙo.
1 Ka hanzarta, ya Allah, ka cece ni;

* **Zabura 69:22** Ko kuwa tarko / zumuncinsu kuma yă zama

Ya UBANGIJI, zo da sauri ka taimake ni.

2 Bari masu neman raina
su sha kunya su kuma rikice;
bari dukan masu sha’awar gani lalacewata
su juye baya da kunya.
3 Bari masu ce mini, “Allah yă ƙara!”
Su juye baya saboda kunyansu.
4 Amma bari dukan masu nemanka
su yi farin ciki su kuma yi murna a cikinka;
bari waɗanda suke ƙaunar cetonka kullum su ce,
“Bari Allah yă sami ɗaukaka!”

5 Duk da haka ni matalauci ne da kuma mai bukata;
ka zo da sauri gare ni, ya Allah.
Kai ne mai taimakona da mai cetona;
Ya UBANGIJI, kada ka yi jinkiri.

# Zabura 71

1 A gare ka, ya UBANGIJI, na nemi mafaka;
kada ka taɓa sa in sha kunya.
2 Ka kuɓutar da ni ka cece ni cikin adalcinka;
ka juya kunnenka gare ni ka kuma cece ni.
3 Ka zama dutsena da kagarata,
inda kullum zan je.
Ka ba da umarni a cece ni,
gama kai ne dutsen ɓuyana da katangata.
4 Ka cece ni, ya Allahna, daga hannun mugaye,
da kuma daga ikon mugaye da masu mugunta.

5 Gama kai ne abin sa zuciyata, ya UBANGIJI Mai Iko Duka,
ƙarfin zuciyata tun ina yaro.
6 Daga haihuwa na dogara gare ka;
kai ka kawo ni daga cikin mahaifiyata.
Kullayaumi zan yabe ka.
7 Na zama kamar abin sa zuciya ga yawanci,
amma kai ne katangata mai ƙarfi.
8 Bakina ya cika da yabonka,
ina furta darajarka dukan yini.

9 Kada ka yar da ni sa’ad da na tsufa;
kada ka yashe ni sa’ad da ƙarfina ya ƙare.
10 Gama abokan gābana suna magana a kaina;
waɗanda suke jira su kashe ni suna haɗa baki tare.
11 Suna cewa, “Allah ya yashe shi;
mu fafare shi mu kama shi,
gama ba wanda zai kuɓutar da shi.”
12 Kada ka yi nisa da ni, ya Allah;
zo da sauri, ya Allahna, ka taimake ni.
13 Bari masu zagina su hallaka da kunya;
bari waɗanda suke so su cutar da ni

su sha ba'a da kuma kunya.

14 Amma game da ni, kullayaumi zan kasance da sa zuciya;
zan yabe ka sau da sau.

15 Bakina zai ba da labarin adalcinka,
zai yi maganar cetonka dukan yini,
ko da yake ban san yawansa ba.
16 Zan zo in furta in kuma yi shelar ayyukanka masu girma, ya UBANGIJI Mai Iko Duka;
zan yi shelar adalcinka, naka kaɗai.
17 Tun ina yaro, ya Allah, ka koya mini
har wa yau ina furta ayyukanka masu banmamaki.
18 Ko sa'ad da na tsufa da furfura,
kada ka yashe ni, ya Allah,
sai na furta ikonka ga tsara mai zuwa,
ƙarfinka ga dukan waɗanda suke zuwa.

19 Adalcinka ya kai sararin sama, ya Allah,
kai da ka yi manyan abubuwa.
Wane ne kamar ka, ya Allah?
20 Ko da yake ka sa na ga wahaloli,
masu yawa da kuma masu ɗaci,
za ka sāke mayar mini da rai;
daga zurfafan duniya
za ka sāke tā da ni.
21 Za ka ƙara girmana
ka sāke ta'azantar da ni.

22 Zan yabe ka da garaya
saboda amincinka, ya Allah;
zan rera yabo gare ka da molo,
Ya Mai Tsarki na Isra'ila.
23 Leɓunana za su yi sowa don farin ciki
sa'ad da na rera yabo gare ka,
ni, wanda ka fansa.
24 Harshena zai ba da labarin ayyukanka masu adalci
dukan yini,
gama waɗanda suka so su cutar da ni
sun sha kunya suka kuma rikice.

# Zabura 72

Ta Solomon.
1 Ka tanada sarki da shari'arka ta gaskiya, ya Allah,
ɗan sarki da adalcinka.
2 Zai* shari'anta mutanenka da adalci,
marasa ƙarfinka da shari'ar gaskiya.

3 Duwatsu za su kawo wadata ga mutane,
tuddai kuma su ba da amfani na adalci.
4 Zai kāre marasa ƙarfi a cikin mutane
yă kuma cece 'ya'yan masu bukata;

* **Zabura 72:2** Ko kuwa Bari yă; daidai da ayoyi 3-11 da kuma 17.

zai murƙushe masu danniya.
5 Zai jimre muddin rana tana nan,
muddin akwai wata, har dukan zamanai.
6 Zai zama kamar ruwan sama mai fāɗuwa a filin ciyayin da aka yanka,
kamar yayyafi mai ba wa duniya ruwa.
7 A kwanakinsa adalai za su haɓaka
wadata za tă yalwata har sai babu sauran wata.

8 Zai yi mulki daga teku zuwa teku
kuma daga Kogi† zuwa iyakar duniya.‡
9 Kabilun hamada za su rusuna a gabansa
abokan gābansa kuwa za su lashe ƙura.
10 Sarakunan Tarshish da na bakin kogi masu nisa
za su ba da gandu gare shi;
sarakunan Sheba da Seba
za su ba shi kyautai.
11 Dukan sarakuna za su rusuna masa
kuma dukan al'ummai za su bauta masa.

12 Gama zai ceci masu bukatan da suka yi kuka,
marasa ƙarfin da ba su da mai taimako.
13 Zai ji tausayin gajiyayyu da masu bukata
yă ceci masu bukata daga mutuwa.
14 Zai kuɓutar da su daga danniya da rikici,
gama jininsu yake a gabansa.

15 Bari yă yi doguwar rayuwa!
Bari a ba shi zinariya daga Sheba.
Bari mutane su riƙa yin addu'a dominsa
su kuma albarkace shi dukan yini.
16 Bari hatsi yă yalwata a duk fāɗin ƙasar;
bari yă cika bisan tuddai.
Bari 'ya'yan itatuwansa su haɓaka kamar Lebanon;
bari yă bazu kamar ciyayi a gona.
17 Bari sunansa yă dawwama har abada;
bari yă ci gaba muddin rana tana nan.

Dukan al'ummai za su sami albarka ta wurinsa,
za su kuma ce da shi mai albarka.

18 Yabo ya tabbata ga Ubangiji Allah, Allah na Isra'ila,
wanda shi kaɗai ya aikata abubuwa masu banmamaki.
19 Yabo ya tabbata ga sunansa mai ɗaukaka har abada;
bari dukan duniya ta cika da ɗaukakarsa.
Amin kuma Amin.

20 Wannan ya kammala addu'o'in Dawuda ɗan Yesse.

## LITTAFI NA UKU

† **Zabura 72:8** Wato, Yuferites ‡ **Zabura 72:8** Ko kuwa iyakar ƙasa

# 73

*Zabura 73–89*
Zabura ta Asaf.
1 Tabbatacce Allah mai alheri ne ga Isra'ila,
ga waɗanda suke masu tsabta a zuciya.

2 Amma game da ni, ƙafafuna suna gab da yin santsi;
tafin ƙafana ya yi kusan zamewa.
3 Gama na yi kishin masu girman kai
sa'ad da na ga cin gaban da masu mugunta suke yi.

4 Ba sa yin wata fama;
jikunansu lafiya suke da kuma ƙarfi.
5 Ba sa shan wata wahalar da sauran mutane ke sha;
ba su da damuwa irin na 'yan adam.
6 Saboda girman kai ya zama musu abin wuya;
tā da hankali ya zama musu riga.
7 Daga mugayen zukatansu laifi kan fito
mugaye ƙulle-ƙullen da suke cikin zukatansu ba su da iyaka.
8 Suna ba'a, suna faɗin mugayen abubuwa;
cikin girman kan suna barazana yin danniya.
9 Bakunansu na cewa sama na su ne,
kuma harsunansu sun mallaki duniya.
10 Saboda haka mutanensu sun juya gare su
suna kuma shan ruwa a yalwace.*
11 Suna cewa, "Yaya Allah zai sani?
Mafi Ɗaukaka yana da sani ne?"

12 Ga yadda mugaye suke,
kullum ba su da damuwa, arzikinsu yana ta ƙaruwa.

13 Tabbatacce a banza na bar zuciyata da tsabta;
a banza na wanke hannuwa don nuna rashin laifi.
14 Dukan yini na sha annoba;
an hukunta ni kowace safiya.

15 Da na ce, "Zan faɗa haka,"
da na bashe 'ya'yanka.
16 Sa'ad da na yi ƙoƙari in gane wannan,
sai ya zama danniya a gare ni
17 sai da na shiga wuri mai tsarki na Allah;
sa'an nan na gane abin da ƙarshensu zai zama.

18 Tabbatacce ka sa su a ƙasa mai santsi;
ka jefar da su ga hallaka.
19 Duba yadda suka hallaka farat ɗaya,
razana ta share su gaba ɗaya!
20 Kamar yadda mafarki yake sa'ad da mutum ya farka,
haka yake sa'ad da ka farka, ya Ubangiji,

---

* **Zabura 73:10** Ba a tabbatar da ma'anar Ibraniyancin da aka yi amfani da shi a wannan aya ba.

za ka rena su kamar almarai.

21 Sa’ad da zuciyata ta ɓaci
hankalina kuma ya tashi,
22 na zama marar azanci da jahili;
na zama kamar dabba a gabanka.

23 Duk da haka kullum ina tare da kai;
ka riƙe ni a hannun damana.
24 Ka bishe ni da shawararka,
bayan haka kuma za ka kai ni cikin ɗaukaka.
25 Wa nake da shi a sama in ba kai ba?
Ba na kuma sha’awar kome a duniya in ban da kai.
26 Jikina da zuciyata za su iya raunana,
amma Allah ne ƙarfin zuciyata
da kuma rabona har abada.

27 Waɗanda suke nesa da kai za su hallaka;
kakan hallaka dukan waɗanda suke maka rashin aminci.
28 Amma game da ni, yana da kyau in kasance kusa da Allah.
Na mai da UBANGIJI Mai Iko Duka mafakata;
zan yi shelar dukan ayyukanka.

# Zabura 74

*Maskil** na Asaf.
1 Me ya sa ka ƙi mu har abada, ya Allah?
Me ya sa fushinka yake a kan tumakin kiwonka?
2 Ka tuna da mutanen da ka saya tun da daɗewa,
kabilar gādonka, wadda ka fansa,
Dutsen Sihiyona, inda ka zauna.
3 Ka juye sawunka wajen waɗannan madawwamin kufai,
dukan wannan hallakar da abokin gāba ya yi wa wuri mai tsarki.

4 Maƙiyanka sun yi ruri a inda ka sadu da mu;
suka kakkafa tutotinsu a matsayin alamu.
5 Sun yi kamar mutane masu wāshin gatura
don yanka itatuwa a kurmi.
6 Sun ragargaje dukan sassaƙar katako
da gatura da kuma gudumarsu.
7 Suka ƙone wurinka mai tsarki ƙurmus;
suka ƙazantar da mazaunin Sunanka.
8 Suna cewa a zukatansu, “Za mu murƙushe su sarai!”
Suka ƙone ko’ina aka yi wa Allah sujada a ƙasar.

9 Ba a ba mu wata alama mai banmamaki ba;
ba sauran annabawan da suka ragu,
kuma babu waninmu da ya sani har yaushe wannan zai ci gaba.
10 Har yaushe abokan gāba za su yi mana ba’a, ya Allah?
Maƙiya za su ci gaba da ɓata sunanka har abada ne?
11 Me ya sa ka janye hannunka, hannunka na dama?
Ka fid da shi daga rigarka ka hallaka su!

* **Zabura 74:** Kan magana, mai yiwuwa kalmar waƙa ce.

12 Amma kai, ya Allah, kai ne sarki tun da daɗewa;
ka kawo ceto a kan duniya.

13 Kai ne ka raba teku ta wurin ikonka;
ka farfashe kawunan dodo a cikin ruwaye.
14 Kai ne ka murƙushe kawunan dodon ruwa
ka kuma ba da shi yă zama abinci ga halittun hamada.
15 Kai ne ka bubbuɗe maɓulɓulai da rafuffuka;
ka busar da koguna masu ruwa.
16 Yini naka ne, dare kuma naka ne;
ka kafa rana da wata.
17 Kai ne ka kafa dukan iyakokin duniya;
ka yi rani da damina.

18 Ka tuna da yadda abokin gāba ya yi maka ba'a, ya UBANGIJI,
yadda wawaye suka ɓata sunanka.
19 Kada ka ba da ran kurciyarka ga namun jeji;
kada ka manta har abada da rayukan mutanenka masu shan azaba.
20 Ka kula da alkawarinka,
domin akwai tashin hankali a kowane lungu mai duhu na ƙasar.
21 Kada ka bar waɗanda ake danniya su sha kunya;
bari matalauta da mabukata su yabe sunanka.
22 Ka tashi, ya Allah, ka kāre muradinka;
ka tuna yadda wawaye suka yi maka ba'a dukan yini.
23 Kada ka ƙyale surutan ban haushi na maƙiyanka,
ihun abokan gābanka, waɗanda suke ci gaba da yi.

# Zabura 75

Don mai bi da kaɗe-kaɗe. Mai muryar "Kada A Hallaka." Zabura ta Asaf. Waƙa ce.

1 Muna maka godiya, ya Allah,
muna maka godiya, gama Sunanka yana kusa;
mutane na faɗin ayyukanka masu banmamaki.

2 Ka ce, "Na zaɓi ƙayyadadden lokaci;
ni ne wanda yake shari'ar gaskiya.
3 Sa'ad da duniya da dukan mutanenta suka girgiza,
ni ne wanda na riƙe ginshiƙan daram.
Sela
4 Ga masu girman kai na ce, 'Kada ku ƙara taƙama,'
ga mugaye kuma, 'Kada ku ɗaga ƙahoninku.
5 Kada ku ɗaga ƙahoninku gāba da sama;
kada ku yi magana da miƙaƙƙen wuya.' "

6 Ba wani daga gabas ko yamma
ko hamada da zai ɗaukaka mutum.
7 Amma Allah ne mai yin shari'a,
yakan saukar da wannan, yă kuma tayar da wani.
8 A hannun UBANGIJI akwai kwaf
cike da ruwan inabi mai kumfa gauraye da kayan yaji;
yakan zuba shi, dukan mugayen duniya kuwa
su sha shi tas.

9 Game da ni dai, zan furta wannan har abada;
zan rera yabo ga Allah na Yaƙub,
10 wanda ya ce, "Zan yanke ƙahonin dukan mugaye,
amma za a ɗaga ƙahonin adalai sama."

# Zabura 76

Don mai bi da kaɗe-kaɗe. Tare da kayan kiɗi masu tsirkiya. Zabura ta Asaf. Waƙa ce.
1 A cikin Yahuda an san Allah;
sunansa da girma yake a cikin Isra'ila.
2 Tentinsa yana a Salem
mazauninsa yana a Sihiyona.
3 A can ya kakkarya kibiyoyin wuta,
garkuwoyi da takuban, makaman yaƙi.
Sela

4 Darajarka tana da haske,
fiye da darajar tuddai waɗanda suke cike da namun jeji masu yawa.
5 Jarumawa sun zube kamar ganima
sun yi barcinsu na ƙarshe;
ba ko jarumi guda
da zai iya ɗaga hannuwansa.
6 A tsawatawarka, ya Allah na Yaƙub,
doki da keken yaƙi suka kwanta ba motsi.

7 Kai kaɗai ne za a ji tsoro.
Wane ne zai iya tsayawa sa'ad da ka yi fushi?
8 Daga sama ka yi shelar hukunci,
ƙasa kuwa ta ji tsoro ta kuwa yi tsit,
9 sa'ad da kai, ya Allah, ka tashi don ka yi shari'a,
don ka cece dukan masu shan wahala a ƙasar.
Sela
10 Tabbatacce fushinka a kan mutane kan jawo maka yabo,
waɗanda suka tsira daga fushinka za su zama kamar rawaninka.

11 Ku yi alkawari wa UBANGIJI Allahnku ku kuma cika su;
bari dukan ƙasashen maƙwabta
su kawo kyautai ga Wannan da za a ji tsoro.
12 Ya kakkarya ƙarfin masu mulki;
sarakunan duniya suna tsoronsa.

# Zabura 77

Don mai bi da kaɗe-kaɗe. Don Yedutun. Na Asaf. Zabura ce.
1 Na yi kuka ga Allah don taimako;
na yi kuka ga Allah don yă ji ni.
2 Sa'ad da nake cikin damuwa, na nemi Ubangiji;
da dare na miƙa hannuwa ba gajiya
raina kuma ya ƙi yă ta'azantu.

3 Na tuna da kai, ya Allah, na kuma yi nishi;
na yi nishi, ƙarfina kuwa duk ya raunana.
Sela

4 ka hana idanuna rufewa;
na damu ƙwarai har ba na iya magana.
5 Na yi tunani kwanakin da suka wuce,
shekarun da suka wuce da daɗewa;
6 na tuna da waƙoƙina da dare.
Zuciyata ta yi nishi, ƙarfina kuwa ya nemi yă sani.

7 “Ubangiji zai ƙi ne har abada?
Ba zai taɓa nuna alherinsa kuma ba?
8 Kaunarsa marar ƙarewa ta ɓace ke nan har abada?
Alkawarinsa ya kāsa ke nan a dukan lokaci?
9 Allah ya manta yă yi jinƙai?
Cikin fushinsa ya janye tausayinsa ne?”

Sela

10 Sai na yi tunani, “Zan yi roƙo saboda wannan,
shekarun da Mafi Ɗaukaka ya miƙa hannunsa na dama.”
11 Zan tuna da ayyukan UBANGIJI;
I, zan tuna mu’ujizanka na tun dā.
12 Zan yi tunani a kan dukan ayyukanka
in lura da dukan manyan abubuwan da ka aikata.

13 Hanyoyinka, ya Allah, masu tsarki ne.
Wanda allah ne yake da girma kamar Allahnmu?
14 Kai ne Allahn da yakan aikata mu’ujizai;
ka nuna ikonka a cikin mutane.
15 Da hannunka mai ƙarfi ka fanshi mutanenka,
zuriyar Yaƙub da Yusuf.

Sela

16 Ruwaye sun gan ka, ya Allah,
ruwaye sun gan ka suka firgita;
zurfafan gaske sun girgiza.
17 Gizagizai sun sauko da ruwa,
sararin sama suka buga tsawa;
kibiyoyinka suka yi ta kai komo da walƙiya.
18 Aka ji tsawanka a cikin guguwa,
walƙiyarka ta haskaka duniya;
duniya ta yi rawar jiki ta girgiza.
19 Hanyarka ta bi ta cikin teku,
hanyarka ta bi cikin manyan ruwaye,
duk da haka ba a ga sawunka ba.

20 Ka bi da mutanenka kamar garke
ta hannun Musa da Haruna.

# Zabura 78

*Maskil** na Asaf.
1 Ya mutanena, ku ji koyarwata;
ku saurari kalmomin bakina.
2 Zan buɗe bakina da misalai,

* **Zabura 78:** Kan magana, mai yiwuwa kalmar waƙa ce.

zan faɗi ɓoyayyun abubuwa, abubuwan dā,
3 abin da muka ji muka kuma sani,
abubuwan da kakanninmu suka faɗa mana.
4 Ba za mu ɓoye su wa ’ya’yanmu ba;
za mu faɗa wa tsara mai zuwa
ayyukan da suka zama yabo na UBANGIJI,
ikonsa, da abubuwan banmamakin da ya aikata.
5 Ya kafa ƙa’idodi wa Yaƙub
ya kuma kafa doka a cikin Isra’ila,
wadda ya umarce kakanni-kakanninmu
su koya wa ’ya’yansu,
6 don tsara na biye su san su,
har da ’ya’yan da ba a riga an haifa ba,
su kuma su faɗa wa ’ya’yansu.
7 Ta haka za su dogara ga Allah
ba kuwa za su manta da ayyukansa ba
amma za su kiyaye umarnansa.
8 Ba za su zama kamar kakanni kakanninsu ba,
masu taurinkai da kuma tsara masu tayarwa,
waɗanda zukatansu ba su yi biyayya ga Allah ba,
waɗanda zukatansu ba su yi aminci ga Allah ba.

9 Mutanen Efraim, ko da yake suna da bakkuna,
suka juya da baya a ranar yaƙi;
10 ba su kiyaye alkawarin Allah ba
suka kuma ƙi su yi rayuwa ta wurin dokarsa.
11 Suka manta da abin da ya aikata,
abubuwan banmamakin da ya nuna musu.
12 Ya yi mu’ujizai a idanun kakanninsu
a ƙasar Masar, a yankin Zowan.
13 Ya raba teku ya kuma bi da su ciki;
ya sa ruwa ya tsaya daram kamar bango.
14 Ya bishe su da girgije da rana
da kuma haske daga wuta dukan dare.
15 Ya tsage duwatsu a cikin hamada
ya kuma ba su ruwaye a yalwace kamar tekuna;
16 ya fid da rafuffuka daga dutsen da ya tsaga
ya sa ruwa ya gudu kamar koguna.

17 Amma suka ci gaba da yin masa zunubi,
suna tayarwa a cikin hamada a kan Mafi Ɗaukaka.
18 Da gangan suka gwada Allah
ta wurin neman abincin da suke kwaɗayi.
19 Suka yi magana a kan Allah,
suna cewa, “Allah zai iya
shimfiɗa tebur a cikin hamada?
20 Sa’ad da ya bugi dutse,
ruwa ya ɓulɓulo,
rafuffuka suka yi gudu a yalwace.
Amma zai iya ba mu abinci?
Zai iya tanada wa mutanensa nama?”

21 Sa'ad da UBANGIJI ya ji su, ya yi fushi ƙwarai;
wutarsa ta ɓarke a kan Yaƙub,
hasalarsa kuwa ta tashi a kan Isra'ila,
22 gama ba su gaskata ga Allah ba
ko su dogara ga cetonsa.
23 Duk da haka ya ba da umarni ga sarari a bisa
ya kuma buɗe ƙofofin sammai;
24 ya sauko da Manna wa mutanensa don su ci,
ya ba su hatsin sama.
25 Mutane suka ci burodin mala'iku;
ya aika musu dukan abincin da za su iya ci.
26 Ya saki iskar gabas daga sammai
ya kuma saki iskar yamma ta wurin ikonsa.
27 Ya sauko da nama a kansu kamar ƙura,
tsuntsaye masu firiya kamar yashi a bakin teku.
28 Ya sa suka sauka a cikin sansaninsu,
ko'ina kewaye da tentunansu.
29 Suka ci har suka sami fiye da abin da ya ishe su,
gama ya ba su abin da suka yi kwaɗayi.
30 Amma kafin su juyo daga abincin da suka yi kwaɗayi,
kai tun ma yana a bakunansu,
31 fushin Allah ya ƙuna a kansu;
ya karkashe waɗanda suka fi ƙiba a cikinsu,
yana yankan matasan Isra'ila.

32 Duk da haka, suka ci gaba da yin zunubi;
duk da abubuwan banmamakinsa, ba su gaskata ba.
33 Saboda haka ya sa kwanakinsu suka ƙare a banza
shekarunsu kuma cikin masifa.
34 A duk sa'ad da Allah ya kashe su, sai su neme shi;
sukan juyo a natse gare shi.
35 Sun tuna cewa Allah ne Dutsensu,
cewa Allah Mafi Ɗaukaka ne Mai fansarsu.
36 Amma sai su yi ta yin masa zaƙin baki,
suna masa ƙarya da harsunansu;
37 zukatansu ba sa biyayya gare shi,
ba su da aminci ga alkawarinsa.
38 Duk da haka ya kasance mai jinƙai;
ya gafarta laifofinsu
bai kuwa hallaka su ba.
Sau da sau ya janye fushinsa
bai kuwa sa fushinsa yǎ ƙuna ba.
39 Ya tuna cewa su naman jiki ne kawai,
iska mai wucewa da ba ta dawowa.

40 Sau da yawa sun tayar masa a cikin hamada
suka kuma ɓata masa rai a jeji!
41 Sau da sau suka riƙa gwada Allah;
suka tsokane Mai Tsarki na Isra'ila.
42 Ba su tuna da ikonsa,
a ranar da ya fanshe su daga mai danniya,

43 ranar da ya nuna mu'ujizansa a Masar
abubuwan banmamakinsa a yankin Zowan ba.
44 Ya mai da kogunansu suka zama jini;
ba su iya sha daga rafuffuka ba.
45 Ya aika da tarin ƙudajen da suka cinye su,
da kwaɗin da suka wahalshe su.
46 Ya ba da hatsinsu ga fāra,
amfanin gonakinsu ga ɗango.
47 Ya lalace inabinsu da ƙanƙara
itatuwan al'ul nasu kuma da jaura.
48 Ya miƙa shanunsu ga ƙanƙara,
tumakinsu ga aradun tsawa.
49 Ya saki musu fushinsa mai zafi,
hasalarsa, zafin rai da kuma ɓacin ransa,
ƙungiyar mala'iku masu hallakarwa.
50 Ya shirya hanya wa fushinsa;
bai tsare ransu daga mutuwa ba
amma ya miƙa su ga annoba.
51 Ya bugi kowane ɗan fari na Masar,
mafari ƙarfin mazantakansu a tentunan Ham.
52 Amma ya fitar da mutanensa kamar garke;
ya bi da su kamar tumaki ta cikin hamada.
53 Ya bi da su lafiya ƙalau, don kada su ji tsoro;
amma teku ya cinye abokan gābansu.
54 Ta haka ya kawo su iyakar ƙasa mai tsarki,
zuwa ƙasar tudun da hannunsa na dama ya kame.
55 Ya kori al'ummai a gabansu
ya rarraba ƙasashensu gare su a matsayin gādo;
ya zaunar da kabilan Isra'ila a gidajensu.

56 Amma suka gwada Allah
suka tayar wa Mafi Ɗaukaka;
ba su kiyaye ƙa'idodinsa ba.
57 Kamar kakanninsu suka zama marasa biyayya da marasa aminci,
marar tabbas kamar tanƙwararren baka.
58 Suka ba shi haushi da masujadansu na kan tudu;
suka tayar da kishinsa da gumakansu.
59 Sa'ad da Allah ya ji su, ya yi fushi ƙwarai;
ya ƙi Isra'ila gaba ɗaya.
60 Ya yashe tabanakul na Shilo,
tentin da ya kafa a cikin mutane.
61 Ya aika da akwatin alkawarin ƙarfinsa zuwa bauta,
darajarsa zuwa cikin hannuwan abokin gāba.
62 Ya ba da mutanensa ga takobi;
ya yi fushi ƙwarai da gādonsa.
63 Wuta ta cinye matasansu maza,
'yan matansu kuma ba su da waƙoƙin aure;
64 aka karkashe firistocinsu,
gwaurayensu kuwa ba su iya makoki ba.

65 Sa'an nan Ubangiji ya farka sai ka ce daga barcinsa,

kamar yadda mutum kan farka daga buguwar ruwan inabi.
66 Ya kori abokan gābansa;
ya sa suka sha madawwamiyar kunya.
67 Sa'an nan ya ƙi tentunan Yusuf,
bai zaɓi kabilar Efraim ba;
68 amma ya zaɓi kabilar Yahuda,
Dutsen Sihiyona, wanda ya ƙaunaci.
69 Ya gina wurinsa mai tsarki kamar bisa,
kamar duniyar da ya kafa har abada.
70 Ya zaɓi Dawuda bawansa
ya kuma ɗauke shi daga ɗakin tumaki;
71 daga kiwon tumaki ya kawo shi
don yă kuma zama makiyayin mutanensa Yaƙub,
na Isra'ila gādonsa.
72 Dawuda kuwa ya zama makiyayinsu da mutuncin zuciya;
da hannuwa masu gwaninta ya bi da su.

# Zabura 79

Zabura ta Asaf.
1 Ya Allah, al'ummai sun mamaye gādonka;
sun ƙazantar da haikalinka mai tsarki,
sun bar Urushalima kufai.
2 Sun ba da gawawwakin bayinka
kamar abinci ga tsuntsayen sararin sama,
nama jikin tsarkakanka ga namun jejin duniya.
3 Sun zubar da jini kamar ruwa
ko'ina a Urushalima,
kuma babu wani da zai binne matattu.
4 Mun zama abin reni ga maƙwabta,
abin ba'a da reni ga waɗanda suke kewaye da mu.

5 Har yaushe, ya Ubangiji za ka yi ta fushi? Har abada ne?
Har yaushe kishinka zai yi ta ƙuna kamar wuta?
6 Ka zuba fushinka a kan al'umman
da ba su yarda da kai ba,
a kan mulkokin
da ba sa kira bisa sunanka;
7 gama sun cinye Yaƙub
suka lalatar da ƙasar zamansa.

8 Kada ka riƙe zunubai kakanni a kanmu;
bari jinƙanka yă zo da sauri yă sadu da mu,
gama mun fid da zuciya sarai.
9 Ka taimake mu, ya Allah Mai Cetonmu,
saboda ɗaukakar sunanka;
ka cece mu ka kuma gafarta mana zunubanmu
saboda sunanka.
10 Don me al'ummai za su ce,
"Ina Allahnsu yake?"

A idanunmu, ka sanar wa al'ummai
cewa kana ɗaukan fansar jinin bayinka da aka zubar.

11 Bari nishe-nishen ʼyan kurkuku su zo gabanka;
ta wurin ƙarfin hannunka ka kiyaye waɗanda aka yanke wa hukuncin mutuwa.
12 Ka sāka a cinyoyin maƙwabtanmu sau bakwai
zage-zagen da suka yi ta yi maka, ya Ubangiji.
13 Saʼan nan mu mutanenka, tumakin makiyayarka,
za mu yabe ka har abada;
daga tsara zuwa tsara
za mu yi ta ba da labarin yabonka.

# Zabura 80

Don mai bi da kaɗe-kaɗe. Mai muryar "Lilin Alkawari." Na Asaf. Zabura ce.
1 Ka ji mu, ya Makiyayin Israʼila,
kai da ka bishe Yusuf kamar garke.
Kai da kake zaune a kursiyi tsakanin kerubobi,
ka haskaka 2 a gaban Efraim, Benyamin da Manasse.
Ka tā da ƙarfinka;
ka zo ka cece mu.

3 Ka mai da mu, ya Allah;
ka sa fuskarka ta haskaka a kanmu,
za mu kuwa cetu.

4 Ya Ubangiji Allah Maɗaukaki,
har yaushe fushinka zai yi ta ƙuna
a kan adduʼoʼin mutanenka?
5 Ka ciyar da su da burodin hawaye;
ka sa suka sha hawaye ta cikakken kwaf.
6 Ka mai da mu abin faɗa ga maƙwabtanmu,
kuma abokan gābanmu suna mana baʼa.

7 Ka mai da mu, ya Allah Maɗaukaki;
ka sa fuskarka ta haskaka a kanmu
za mu kuwa cetu.

8 Ka fitar da inabi daga Masar;
ka kori alʼummai ka kuma dasa shi.
9 Ka gyara wuri saboda shi,
ya kuwa yi saiwa ya cike ƙasa.
10 Aka rufe duwatsu da inuwarsa,
manya-manyan itatuwan alʼul da rassansa.
11 Ya miƙe rassansa zuwa Teku
tohonsa har zuwa Kogi.

12 Me ya sa ka rurrushe bangayensa
don duk masu wucewa su tsinke ʼyaʼyan inabinsa?
13 Aladu daga kurmi suna ɓarnatar da shi
halittun gonaki kuma suna cinsa.
14 Ka komo wurinmu, ya Allah Maɗaukaki!
Ka duba daga sama ka gani!
Ka lura da wannan inabi,
15 saiwar da hannun damarka ya dasa,
ɗan da ka renar wa kanka.

16 An yanke inabinka, an ƙone shi da wuta;
a tsawatawarka mutanenka sun hallaka.
17 Bari hannunka yă zauna a kan mutumin da yake hannun damarka,
ɗan mutum da ka renar wa kanka.
18 Ta haka ba za mu juye mu bar ka ba;
ka rayar da mu, za mu kuwa kira bisa sunanka.

19 Ka mai da mu, ya UBANGIJI Allah Maɗaukaki;
ka sa fuskarka ta haskaka a kanmu,
za mu kuwa cetu.

# Zabura 81

Don mai bi da kaɗe-kaɗe. Bisa ga *gittit.** Ta Asaf.
1 Ku rera don farin ciki ga Allah ƙarfinmu;
ku yi sowa ga Allah na Yaƙub!
2 Ku fara kaɗe-kaɗe, ku buga ganga,
ku kaɗa garaya da molo masu daɗi.

3 Ku busa ƙahon rago a Sabon Wata,
da kuma sa'ad da wata ya kai tsakiya, a ranar Bikinmu;
4 wannan ƙa'ida ce domin Isra'ila,
farilla ta Allah na Yaƙub.
5 Ya kafa shi a matsayin ƙa'ida domin Yusuf
sa'ad da ya fito daga Masar.

Muka ji yaren da ba mu fahimta ba.

6 Ya ce, "Na kau da nauyi daga kafaɗunku;
an 'yantar da hannuwansu daga kwando.
7 Cikin damuwarku kun yi kira na kuwa kuɓutar da ku,
na amsa muku daga girgijen tsawa;
na gwada ku a ruwan Meriba.

Sela

8 "Ku ji, ya mutanena, zan kuwa gargaɗe ku,
in ba za ku saurare ni ba, ya Isra'ila!
9 Kada ku kasance da baƙon allah a cikinku;
ba za ku rusuna ga baƙon allah ba.
10 Ni ne UBANGIJI Allahnku
wanda ya fitar da ku daga Masar.
Ku buɗe bakinku zan kuwa cika shi.

11 "Amma mutanena ba su saurare ni ba;
Isra'ila bai miƙa kansa gare ni ba.
12 Saboda haka na ba da su ga zukatansu da suka taurare
don su bi dabararsu.

13 "A ce mutanena za su saurare ni,
a ce Isra'ila zai bi hanyoyina,
14 da nan da nan sai in rinjayi abokan gābansu
in kuma juye hannuna a kan maƙiyansu!

* **Zabura 81:** Kan magana, mai yiwuwa wata kalmar waƙa ce.

15 Waɗanda suke ƙin UBANGIJI za su fāɗi a gabansa da rawar jiki,
hukuncinsu kuma zai dawwama har abada.
16 Amma za a ciyar da ku da alkama mafi kyau;
da zuma daga dutsen da zai ƙosar da ku."

# Zabura 82

Zabura ta Asaf.
1 Allah yana shugabanta cikin babban taro;
yakan zartar da hukunci a cikin "alloli".

2 "Har yaushe za ku kāre marasa adalci
ku kuma goyi bayan mugaye?
Sela
3 Ku tsare mutuncin marasa ƙarfi da marayu;
ku kāre hakkin matalauta da waɗanda ake danniya.
4 Ku ceci marasa ƙarfi da masu bukata;
ku kuɓutar da su daga hannun mugaye.

5 "Ba su san kome ba, ba su fahimci kome ba.
Suna yawo cikin duhu;
an girgiza dukan tussan duniya.

6 "Na ce, 'Ku "alloli" ne;
dukanku 'ya'yan Mafi Ɗaukaka' ne.
7 Amma za ku mutu kamar mutum kurum;
za ku fāɗi kamar duk wani mai mulki."

8 Ka tashi, ya Allah, ka shari'anta duniya,
gama dukan al'ummai gādonka ne.

# Zabura 83

Waƙa ce. Zabura ta Asaf.
1 Ya Allah, kada ka yi shiru;
kada ka tsaya cik,
ya Allah, kada ka daina motsi.
2 Dubi yadda abokan gābanka suke fariya,
dubi yadda maƙiyanka suke ɗaga kansu.
3 Da wayo suna ƙulle-ƙulle a kan mutanenka;
suna shirya maƙarƙashiya a kan waɗanda kake so.
4 Suna cewa, "Ku zo, bari mu hallaka su ɗungum a matsayin al'umma,
don kada a ƙara tuna da sunan Isra'ila."

5 Da zuciya ɗaya suka yi ƙulle-ƙulle tare;
suka haɗa kai gāba da kai,
6 tentunan Edom da na mutanen Ishmayel,
na Mowab da kuma na Hagirawa,
7 Gebal, Ammon da Amalek,
Filistiya, tare da mutanen Taya.
8 Har Assuriya ma ta haɗa kai da su
don ta ba da ƙarfi ga zuriyar Lot.
Sela

9 Ka yi musu abin da ka yi wa Midiyan,
yadda ka yi wa Sisera da Yabin a kogin Kishon,
10 waɗanda suka hallaka a En Dor
suka zama kamar juji a ƙasa.
11 Ka mai da manyansu kamar Oreb da Zeyib,
dukan sarakunansu kamar Zeba da Zalmunna,
12 waɗanda suka ce, "Bari mu mallaki
wuraren kiwon Allah."

13 Ka mai da su kamar ɗan tsiron da kan karye, iska ta yi ta turawa, ya Allahna,
kamar yayin da iska take hurawa,
14 kamar yadda wuta ke cin kurmi
ko harshen wutar da take ci a kan duwatsu,
15 haka za ka kore su da iska mai ƙarfi
ka kuma firgita su da guguwarka.
16 Ka rushe fuskokinsu da kunya
don mutane su nemi sunanka, ya UBANGIJI.

17 Bari su kasance cikin kunya da taƙaici;
bari su hallaka cikin wulaƙanci.
18 Bari su san cewa kai, wanda sunansa ne UBANGIJI,
cewa kai kaɗai ne Mafi Ɗaukaka a bisa dukan duniya.

# Zabura 84

Don mai bi da kaɗe-kaɗe. Bisa ga *gittit.** Na 'Ya'yan Kora maza. Zabura ce.

1 Ina misalin kyan wurin zamanka,
Ya UBANGIJI Maɗaukaki!
2 Raina yana marmari, har yana suma,
don filayen gidan UBANGIJI;
zuciyata da namana na tā da murya
domin Allah mai rai.
3 Har tsada ma ta sami gida,
tsatsewa kuma ta yi wa kanta sheƙa,
inda za tă ƙyanƙyashe 'ya'yanta,
wuri kusa da bagadenka,
Ya UBANGIJI Maɗaukaki, Sarkina da kuma Allahna.
4 Masu albarka ne waɗanda suke zama a gidanka;
kullum suna ta yabonka.

Sela

5 Masu albarka ne waɗanda ƙarfinsu yana daga gare ka,
waɗanda suka kafa zukatansu a yin tafiya zuwa wuri mai tsarki ne.
6 Yayinda suke wuce ta Kwarin Baka,
sukan mai da shi wurin maɓulɓulai;
ruwan sama na farko kuma kan rufe shi da tafkuna.
7 Suna ta ƙara ƙarfi,
har sai kowanne ya bayyana a gaban Allah a Sihiyona.

8 Ka ji addu'ata, ya UBANGIJI Allah Maɗaukaki;
ka saurare ni, ya Allah na Yaƙub.

Sela

* **Zabura 84:** Kan magana, mai yiwuwa wata kalmar waƙa ce.

9 Ka dubi garkuwarmu, ya Allah;
ka duba da alheri a kan shafaffenka.

10 Rana guda a filayen gidan sun fi
dubu a wani wuri dabam;
zan gwammaci in zama mai tsaron ƙofa a gidan Allahna
da in zauna a tentunan mugaye.
11 Gama UBANGIJI Allah rana ne da kuma garkuwa;
UBANGIJI yakan yi alheri da kuma daraja;
ba ya hana kowane abu mai kyau
wa waɗanda suke aikata abin da yake daidai.

12 Ya UBANGIJI Maɗaukaki,
mai albarka ne mutumin da ya dogara gare ka.

# Zabura 85

Don mai bi da kaɗe-kaɗe. Na 'ya'yan Kora maza. Zabura ce.
1 Ka nuna wa ƙasarka alheri, ya UBANGIJI;
ka mai da nasarorin Yaƙub.
2 Ka gafarta laifin mutanenka
ka kuma shafe dukan zunubansu.
Sela
3 Ka kau da dukan fushinka
ka kuma juye daga hasalar fushinka.

4 Ka sāke mai da mu, ya Allah Mai Cetonmu,
ka kau da rashin jin daɗinka daga gare mu.
5 Za ka ci gaba da fushi da mu har abada ne?
Za ka ja fushinka cikin dukan tsararraki?
6 Ba za ka sāke raya mu ba,
don mutanenka su yi farin ciki a cikinka?
7 Ka nuna mana ƙaunarka marar ƙarewa, ya UBANGIJI,
ka kuma ba mu cetonka.

8 Zan saurari abin da Allah UBANGIJI zai faɗa;
ya yi alkawarin salama ga mutanensa, tsarkakansa,
amma kada su koma ga wauta.
9 Tabbatacce cetonsa yana kusa da waɗanda suke tsoronsa,
don ɗaukakarsa ta zauna a cikin ƙasarmu.

10 Kauna da aminci za su sadu;
adalci da salama za su yi wa juna sumba.
11 Aminci zai ɓulɓulo daga ƙasa,
adalci kuma yă duba daga sama.
12 UBANGIJI tabbatacce zai bayar da abin da yake da kyau,
ƙasarmu kuwa za tă ba da amfaninta.
13 Adalci na tafiya a gabansa
yana shirya hanya domin ƙafafunsa.

# Zabura 86

Addu'ar Dawuda.
1 Ka ji, ya UBANGIJI, ka kuma amsa mini,

gama ni matalauci ne mai bukata kuma.
2 Ka tsare raina, gama na ba da kaina gare ka.
Kai ne Allahna; ka ceci bawanka
wanda ya dogara gare ka.
3 Ka yi mini jinƙai, ya Ubangiji,
gama na yi kira gare ka dukan yini.
4 Ka ba bawanka farin ciki
gama gare ka, ya Ubangiji,
na miƙa raina.

5 Kai mai gafartawa da kuma mai alheri ne, ya Ubangiji,
cike da ƙauna ga dukan waɗanda suke kira gare ka.
6 Ka ji addu'ata, ya UBANGIJI;
ka saurari kukata na neman jinƙai.
7 A lokacin wahala zan yi kira gare ka,
gama za ka amsa mini.

8 A cikin alloli babu kamar ka, ya Ubangiji;
babu ayyukan da za a kwatanta da naka.
9 Dukan al'umman da ka yi
za su zo su yi sujada a gabanka, ya Ubangiji;
za su kawo ɗaukaka ga sunanka.
10 Gama kai mai girma ne kana kuma aikata ayyuka masu banmamaki;
kai kaɗai ne Allah.

11 Ka koya mini hanyarka, ya UBANGIJI,
zan kuwa yi tafiya cikin gaskiyarka;
ka ba ni zuciya wadda ba tǎ rabu ba,
don in ji tsoron sunanka.
12 Zan yabe ka, ya Ubangiji Allahna, da dukan zuciyata;
zan ɗaukaka sunanka har abada.
13 Gama ƙaunarka da girma take gare ni;
kai ka cece ni daga zurfafa,
daga mazaunin matattu.

14 Masu girman kai suna kai mini hari, ya Allah;
ƙungiyar marasa imani suna neman raina,
mutanen da ba su kula da kai ba.
15 Amma kai, ya Ubangiji, kai Allah mai tausayi ne da kuma mai alheri,
mai jinkirin fushi, mai yawan ƙauna da aminci.
16 Ka juyo gare ni ka yi mini jinƙai;
ka ba wa bawanka ƙarfi;
ka ceci ni gama na bauta maka
yadda mahaifiyata ta yi.
17 Ka ba ni alamar alherinka,
don abokan gābana su gani su kuma sha kunya,
gama kai, ya UBANGIJI, ka taimake ni ka kuma ta'azantar da ni.

# Zabura 87

Na 'ya'yan Kora maza. Zabura ce. Waƙa ce.
1 Ya kafa harsashinsa a kan dutse mai tsarki.
2 UBANGIJI yana ƙaunar ƙofofin Sihiyona

fiye da dukan wuraren zaman Yaƙub.

3 Ana faɗin abubuwa masu ɗaukaka game da ke
Ya birnin Allah,
Sela
4 "Zan lissafta Rahab
a cikin waɗanda suka san ni,
Filistiya ita ma, da Taya, tare da Kush,
zan kuma ce, 'An haifi wannan a Sihiyona.' "
5 Tabbatacce, game da Sihiyona za a ce,
"Wannan da wancan an haifa a cikinta,
Mafi Ɗaukaka kansa zai kafa ta."
6 UBANGIJI zai rubuta a littafin sunayen mutanensa,
"An haifi wannan a Sihiyona."
Sela

7 Yayinda suke kaɗe-kaɗe za su rera,
"Dukan maɓulɓulaina suna cikinki."

# Zabura 88

Waƙa ce, Zabura ta 'ya'yan Kora maza. Don mai bi da kaɗe-kaɗe. Bisa ga *mahalat leyannot** *maskil*† na Heman dangin Ezra.

1 Ya UBANGIJI, Allah wanda ya cece ni,
dare da rana ina kuka a gabanka.
2 Bari addu'ata ta zo a gabanka;
ka kasa kunne ga kukata.

3 Gama raina yana cike da wahala
rayuwata tana gab da kabari.‡
4 An lissafta ni cikin waɗanda suka gangara zuwa cikin rami;
ni kamar mutumin da ba shi da ƙarfi ne.
5 An ware ni tare da matattu,
kamar waɗanda aka kashe da suke kwance a kabari,
waɗanda ba ka ƙara tunawa,
waɗanda aka yanke daga taimakonka.

6 Ka sa ni a ramin da yake can ƙasa
cikin zurfafa mafi duhu.
7 Hasalarka tana da nauyi a kaina;
ka turmushe ni da dukan raƙumanka.
Sela
8 Ka ɗauke abokaina na kurkusa daga gare ni
ka sa na zama abin ƙyama a gare su.
An kange ni, ba yadda zan kuɓuta
9 idanuna ba sa gani sosai saboda baƙin ciki.

Ina kira gare ka, ya UBANGIJI, kowace rana;
na tā da hannuwana zuwa gare ka.
10 Kakan nuna wa matattu ayyukanka na banmamaki ne?
Waɗanda suka mutu sukan tashi su yabe ka ne?

---

* **Zabura 88:** Kan magana, mai yiwuwa muryar "Tsananin Baƙin Ciki." † **Zabura 88:** Kan magana, mai yiwuwa kalma waƙa ce. ‡ **Zabura 88:3** Da Ibraniyanci Sheol

Sela

11 Ana furta ƙaunar a cikin kabari ne,
ana zancen amincinka a cikin Hallaka ne?
12 An san ayyukanka masu banmamaki a wurin duhu ne,
ko ayyukan adalcinka a lahira?

13 Amma ina kuka gare ka neman taimako, ya UBANGIJI;
da safe addu'ata kan zo gabanka.
14 Don me, ya UBANGIJI, ka ƙi ni
ka kuma ɓoye fuskarka daga gare ni?

15 Tun ina ƙarami na sha wahala na kuma yi kusa in mutu;
na sha wahalar razanarka kuma na kuma fid da zuciya.
16 Hasalarka ta sha kaina;
razanarka ta hallaka ni.
17 Dukan yini sun kewaye ni kamar rigyawa;
sun mamaye ni ɗungum.
18 Ka ɗauke abokaina da ƙaunatattuna daga gare ni;
duhu ne abokina na kurkusa.

# Zabura 89

*Maskil** na Etan dangin Ezra.

1 Zan rera game da ƙauna mai girma ta UBANGIJI har abada;
da bakina zan sanar da amincinka
a dukan zamanai.
2 Zan furta cewa ƙaunarka tana nan daram har abada,
cewa ka kafa amincinka a sama kanta.
3 Ka ce, "Na yi alkawari da zaɓaɓɓena,
na rantse wa Dawuda bawana,
4 cewa 'Zan kafa zuriyarka har abada
in kuma sa kursiyinka yǎ tsaya daram dukan zamanai.' "

Sela

5 Sammai na yabon abubuwan banmamakinka, ya UBANGIJI,
amincinka shi ma, a cikin taron tsarkakanka.
6 Gama wane ne a sarari za a iya kwatanta da UBANGIJI?
Wane ne yake kamar UBANGIJI a cikin talikan samaniya?
7 Cikin taron tsarkaka Allah ne aka fi tsoro;
shi ne mafi bantsoro fiye da dukan waɗanda suka kewaye shi.
8 Ya UBANGIJI Allah Maɗaukaki, wane ne kamar ka?
Kai mai iko ne, ya UBANGIJI, kuma amincinka ya kewaye ka.

9 Kana mulkin teku mai tumbatsa;
sa'ad da raƙuma sun tashi, kakan kwantar da su.
10 Ka ragargaza Rahab kamar waɗanda aka kashe;
da hannunka mai ƙarfi ka watsar da abokan gābanka.
11 Sammai naka ne, haka kuma duniya;
ka kafa duniya da dukan abin da yake cikinta.
12 Ka halicce arewa da kudu;
Tabor da Hermon suna rera don farin ciki ga sunanka.
13 Hannunka mai iko ne;

* **Zabura 89:** Kan magana, mai yiwuwa kalmar waƙa ce.

hannunka yana da ƙarfi, hannunka na dama ya sami ɗaukaka.

14 Adalci da gaskiya su ne tushen kursiyinka;
ƙauna da aminci suna tafiya a gabanka.
15 Masu albarka ne waɗanda suka koyi yin maka kirari
waɗanda suke tafiya cikin hasken da yake gabanka, UBANGIJI.
16 Suna farin ciki a cikin sunanka dukan yini;
suna samun ɗaukaka cikin adalcinka.
17 Gama kai ne ɗaukakarsu da ƙarfinsu,
kuma ta wurin alherinka ka ɗaukaka ƙahonka.†
18 Tabbatacce, garkuwarmu ta UBANGIJI ce,
ta sarkinmu ce, da kuma ta Mai Tsarki na Isra'ila ce.

19 Ka taɓa yin magana cikin wahayi,
ga mutanenka masu aminci ka ce,
"Na ba wa jarumi ƙarfi;
na ɗaukaka saurayi daga cikin mutane.
20 Na sami Dawuda bawana;
da mai na mai tsarki na shafe shi.
21 Hannuna zai kasance tare da shi;
tabbatacce hannuna zai ƙarfafa shi.
22 Babu abokin gāban da zai sa yă biya haraji;
babu mugun mutumin da zai danne shi.
23 Zan murƙushe maƙiyansa a gabansa
in kashe dukan abokan gābansa.
24 Amintacciya ƙaunata za tă kasance tare da shi,
kuma ta wurin sunana za a ɗaukaka ƙahonsa.
25 Zan sa hannunsa a bisa teku,
hannunsa na dama a bisa koguna.
26 Zai yi kira gare ni yă ce, 'Kai ne Mahaifina,
Allahna, Dutse mai cetona.'
27 Zan kuma naɗa shi ɗan farina,
mafi ɗaukaka cikin sarakunan duniya.
28 Zan ci gaba da ƙaunarsa har abada,
alkawarina da shi ba zai taɓa fasa ba.
29 Zan kafa zuriyarsa har abada,
kursiyinsa muddin sammai suna nan.

30 "In 'ya'yansa maza suka yashe dokata
ba su kuwa bi ƙa'idodina ba,
31 in suka take ƙa'idodina
suka kuma kāsa kiyaye umarnaina,
32 zan hukunta zunubinsu da sanda,
laifinsu da bulala;
33 amma ba zan ɗauke ƙaunata daga gare shi ba,
ba kuwa zan taɓa rasa cika amincina ba.
34 Ba zan take alkawarina ba
ko in canja abin da leɓunana suka ambata.
35 Sau ɗaya ba ƙari, na rantse da tsarkina,
ba kuwa zan yi ƙarya wa Dawuda ba,
36 cewa zuriyarsa za tă ci gaba har abada

† **Zabura 89:17** ƙaho a nan na kwatanta mai ƙarfi.

kuma kursiyinsa zai dawwama a gabana kamar rana;
37 zai kahu har abada kamar wata,
amintacciyar shaida a cikin sarari."

Sela

38 Amma ka ƙi, ka yi ƙyama
ka kuma yi fushi sosai da shafaffenka.
39 Ka soke alkawarin da ka yi da bawanka
ka kuma ƙazantar da rawaninsa a ƙura.
40 Ka rurrushe dukan katangansa
ka sa kagaransa suka zama kufai.
41 Dukan waɗanda suka wuce sun washe shi;
ya zama abin dariya wajen maƙwabtansa.
42 Ka ɗaukaka hannun dama na maƙiyansa;
ka sa dukan abokan gābansa suna farin ciki.
43 Ka juye bakin takobinsa
ba ka kuma taimake shi a cikin yaƙi ba.
44 Ka kawo ƙarshen darajarsa
ka kuma jefar da kursiyinsa ƙasa.
45 Ka rage kwanakin ƙuruciyarsa;
ka rufe shi da mayafin kunya.

Sela

46 Har yaushe, ya Ubangiji za ka ɓoye? Za ka ɓoye har abada ne?
Har yaushe fushinka zai yi ta ci kamar wuta?
47 Ka tuna yadda raina mai wucewa ne.
Gama ka halicce dukan mutane ba amfani!
48 Wanda mutum ne zai rayu da ba zai ga mutuwa ba,
ko yǎ cece kansa daga ikon kabari?

Sela

49 Ya Ubangiji, ina ƙaunar mai girma ta dā,
wadda cikin amincinka ka rantse wa Dawuda?
50 Ka tuna, Ubangiji, yadda aka yi wa bawanka ba'a,
yadda na jimre a zuciyata da zage-zagen dukan al'ummai,
51 zage-zagen da abokan gābanka suka yi mini, ya Ubangiji,
da suka yi wa kowane matakin da shafaffenka ya ɗauka.

52 Yabo ya tabbata ga Ubangiji har abada!
Amin kuma Amin.

# LITTAFI NA HUƊU

## 90

*Zabura 90–106*

Addu'ar Musa Mutumin Allah.
1 Ubangiji kai ne mazauninmu
cikin dukan zamanai.
2 Kafin a haifi duwatsu
ko a fid da ƙasa da duniya,
daga madawwami zuwa madawwami kai Allah ne.

3 Ka komar da mutane zuwa ƙura,
kana cewa, "Ku koma ƙura, ya ku 'ya'yan mutane."

4 Gama shekaru dubu a gabanka
kamar kwana ɗaya ne da ya wuce,
ko sa'a guda na dare.
5 Ka share mutane cikin barcin mutuwa;
suna kama da sabuwa ciyawar safiya,
6 ko da yake da safe takan yi sabuwar huda
da yamma sai ta bushe ta kuma yanƙwane.

7 An cinye mu ta wurin fushinka
mun kuma razana ta wurin hasalarka.
8 Ka ajiye laifinmu a gabanka,
asirin zunubanmu a hasken kasancewarka.
9 Dukan kwanakinmu sun wuce ƙarƙashin fushinka;
mun gama shekarunmu da nishi.
10 Tsawon kwanakinmu shekaru saba'in ne,
ko tamanin, in muna da ƙarfi;
duk da haka tsawonsu wahaloli ne kawai da ɓacin rai,
gama da sauri suke wucewa, ta mu kuma ta ƙare.
11 Wa ya san ƙarfin fushinka?
Gama hasalarka tana da girma kamar tsoron da ya dace da kai.
12 Ka koya mana yawan kwanakinmu daidai,
don mu sami zuciyar hikima.

13 Ka ji mu, ya UBANGIJI! Har yaushe zai ci gaba?
Ka ji tausayin bayinka.
14 Ka ƙosar da mu da safe da ƙaunarka marar ƙarewa,
don mu rera don yabo, mu kuma yi murna dukan kwanakinmu.
15 Faranta mana zuciya kamar yawan kwanakin da muka sha azaba,
kamar yawan shekarun da muka ga wahala.
16 Bari a nuna ayyukanka ga bayinka,
darajarka ga 'ya'yansu.

17 Bari alherin shugabanmu Allah yă kasance a kanmu;
ka albarkaci mana aikin hannuwanmu,
I, ka albarkaci aikin hannuwanmu.

# Zabura 91

1 Shi wanda yake zama a wurin Mafi Ɗaukaka
zai huta a cikin inuwar Maɗaukaki.*
2 Zan ce game da UBANGIJI, "Shi ne mafakata da kagarata,
Allahna, wanda nake dogara."

3 Tabbatacce zai cece ka
daga tarkon mai farauta
da kuma daga cututtuka masu kisa.
4 Zai rufe ka da fikafikansa,
a ƙarƙashin fikafikansa kuwa za ka sami mafaka;
amincinsa zai zama maka garkuwa da katanga.
5 Ba za ka ji tsoron razanar dare,
ko kibiyoyi da suke firiya da rana ba,
6 ko bala'in da yake aukowa cikin duhu,

* **Zabura 91:1** Da Ibraniyanci Shaddai

ko annobar da take hallakarwa da tsakar rana.
7 Dubu za su iya fāɗuwa a gefenka,
dubu goma a hannun damanka,
amma ba abin da zai zo kusa da kai.
8 Za ka dai gan da idanunka
yadda ake hukunta mugaye.

9 In ka mai da Mafi Ɗaukaka wurin zamanka,
har ma UBANGIJI wanda yake mafakata,
10 to, babu wani mugun abin da zai same ka,
ba masifar da za tă zo kusa da tentinka.
11 Gama zai umarci mala'ikunsa game da kai
don su tsare ka a dukan hanyoyinka;
12 za su tallafe ka da hannuwansu,
don kada ka buga ƙafarka a kan dutse.
13 Za ka taka zaki da gamsheƙa;
za ka tattake babban zaki da maciji.

14 UBANGIJI ya ce, "Domin ya ƙaunace ni, zan kuɓutar da shi;
zan kiyaye shi, gama ya yarda da sunana.
15 Zai kira bisa sunana, zan kuma amsa masa;
zan kasance tare da shi a lokacin wahala,
zan kuɓutar da shi in kuma girmama shi.
16 Da tsawon rai zan ƙosar da shi
in kuma nuna masa cetona."

# Zabura 92

Zabura ce. Waƙa ce. Domin ranar Asabbaci.
1 Yana da kyau a yabi UBANGIJI
a kuma yi kiɗi ga sunanka, ya Mafi Ɗaukaka,
2 don a yi shelar ƙaunarka da safe
amincinka kuma da dare,
3 da kiɗin molo mai tsirkiya goma
da kuma ƙarar garaya.

4 Gama ka sa na yi murna ta wurin ayyukanka, ya UBANGIJI;
na rera don farin ciki saboda ayyukan hannuwanka.
5 Ina misalin ayyukanka, ya UBANGIJI,
tunaninka da zurfi suke ƙwarai!
6 Mutum marar azanci ba zai sani ba,
wawa ba zai gane ba,
7 cewa ko da yake mugaye suna girma kamar ciyawa
kuma dukan masu aikata mugunta suna haɓaka,
za a hallaka su har abada.

8 Amma kai, ya UBANGIJI, za a ɗaukaka har abada.

9 Gama tabbatacce abokan gābanka, ya UBANGIJI,
tabbatacce abokan gābanka za su hallaka;
za a watsar da dukan masu aikata mugunta.
10 Ka ɗaukaka ƙahona kamar na ɓauna;
an zubo mai masu kyau a kaina.

11 Idanuna sun ga fāɗuwar maƙiyana;
kunnuwana sun ji kukan mugayen maƙiyana.

12 Adalai za su haɓaka kamar itacen dabino,
za su yi girma kama al'ul na Lebanon;
13 da aka daddasa a gidan UBANGIJI,
za su haɓaka a filayen gidan Allahnmu.
14 Za su ci gaba da ba da 'ya'ya a tsufansu,
za su kasance ɗanye kuma kore shar,
15 suna shela cewa, "UBANGIJI adali ne;
shi ne Dutsena, kuma babu mugunta a cikinsa."

# Zabura 93

1 UBANGIJI yana mulki, yana sanye da ɗaukaka;
UBANGIJI yana sanye da ɗaukaka yana kuma sanye da ƙarfi.
An kafa duniya daram; ba za a iya matsar da ita ba.
2 An kafa kursiyin tun da daɗewa;
kana nan tun fil azal.

3 Tekuna sun taso, ya UBANGIJI,
tekuna sun ta da muryarsu;
tekuna sun tā da ta raƙumansu masu tumbatsa.
4 Mafi ƙarfi fiye da tsawan manyan ruwaye,
mafi ƙarfi fiye da ikon raƙuman ruwan teku,
UBANGIJI mai zama a bisa mai girma ne.

5 Ka'idodinka suna nan daram;
tsarki ya yi wa gidanka ado
har kwanaki marar ƙarewa, ya UBANGIJI.

# Zabura 94

1 Ya UBANGIJI, Allahn da yake ramuwa,
Ya Allah wanda yake ramuwa, ka haskaka.
2 Ka tashi, ya Alƙalin duniya;
ka sāka wa masu girman kai abin da ya dace da su.
3 Har yaushe mugaye, ya UBANGIJI
har yaushe mugaye za su yi ta murna?

4 Suna ta yin maganganun fariya;
dukan masu aikata mugunta sun cika da fariya.
5 Suna murƙushe mutanenka, ya UBANGIJI;
suna danne gādonka.
6 Suna kashe gwauraye da kuma baƙi;
suna kisan marayu.
7 Suna ce, "UBANGIJI ba ya gani;
Allah na Yaƙub bai kula ba."

8 Ku mai da hankali, ku marasa azanci a cikin mutane;
ku wawaye, yaushe za ku zama masu hikima?
9 Shi da ya sa kunne ba don a ji ba ne?
Shi da ya yi ido ba don yă gani ba ne?

10 Shi da yake yi wa al'ummai horo ba ya hukunci ne?
Shi da yake koya wa mutum ba shi da sani ne?
11 UBANGIJI ya san tunanin mutum;
ya san cewa tunaninsu banza ne.

12 Mai albarka ne mutumin da ka yi masa horo, ya UBANGIJI,
mutumin da ka koyar daga dokarka;
13 kana ba shi sauƙi a lokacin wahala,
sai har an haƙa rami wa mugaye.
14 Gama UBANGIJI ba zai ƙi mutanensa ba;
ba zai taɓa yashe gādonsa ba.
15 Za a sāke kafa hukunci a kan adalci,
kuma dukan masu adalci a zuciya za su bi shi.

16 Wane ne zai yi gāba da mugaye domina?
Wane ne zai ɗauki matsayi ya yi gāba da masu aikata mugunta domina?
17 Da ba don UBANGIJI ya yi mini taimako ba,
da tuni na zauna shiru a wurin mutuwa.
18 Sa'ad da na ce, "Kafata na santsi,"
ƙaunarka, ya UBANGIJI, ta riƙe ni.
19 Sa'ad da alhini ya yi yawa a cikina,
ta'aziyyarka ta kawo farin ciki wa raina.

20 Zai yiwu kursiyin da ya cika da lalaci yă haɗa kai da kai,
wanda yake kawo azaba ta wurin abin da ya zartar?
21 Sun yi ƙungiya tare a kan mai adalci
suka yanke wa marar laifi hukuncin mutuwa.
22 Amma UBANGIJI ya zama kagarata,
Allahna kuma dutsen da nake samun mafaka.
23 Zai sāka musu saboda zunubansu
yă kuma hallaka su saboda muguntarsu;
UBANGIJI Allahnmu zai hallaka su.

# Zabura 95

1 Ku zo, bari mu rera don farin ciki ga UBANGIJI;
bari mu yi sowa da ƙarfi ga Dutsen cetonmu.
2 Bari mu zo gabansa da godiya
mu rera gare shi da kiɗi da waƙa.

3 Gama UBANGIJI Allah mai girma ne,
babban Sarki a bisa dukan alloli.
4 A hannunsa ne zurfafan duniya suke,
ƙwanƙolin dutse kuma nasa ne.
5 Teku nasa ne, gama shi ne ya yi shi,
da hannuwansa kuma ya yi busasshiyar ƙasa.

6 Ku zo, bari mu rusuna mu yi sujada,
bari mu durƙusa a gaban UBANGIJI Mahaliccinmu;
7 gama shi ne Allahnmu
mu mutanen makiyayansa ne,
garke kuwa a ƙarƙashin kulawarsa.

Yau, in kuka ji muryarsa,
8 “Kada ku taurare zukatanku kamar yadda kuka yi a Meriba,*
kamar yadda kuka yi a wancan rana a Massa† a hamada,
9 inda kakanninku suka gwada suka kuma jarraba ni,
ko da yake sun ga abin da na yi.
10 Shekara arba’in na yi fushi da wancan tsara;
na ce, ‘Su mutane ne waɗanda zukatansu suka kauce,
kuma ba su san hanyoyina ba.’
11 Saboda haka na yi rantsuwa cikin fushina,
‘Ba za su taɓa shiga hutuna ba.’ ”

# Zabura 96

1 Ku rera sabuwar waƙa ga UBANGIJI;
ku rera ga UBANGIJI, ku duniya duka.
2 Ku rera ga UBANGIJI, ku yabe sunansa;
ku yi shelar cetonsa kowace rana.
3 Ku furta ɗaukakarsa a cikin al’ummai,
manyan ayyukansa a cikin dukan mutane.

4 Gama da girma UBANGIJI yake, ya kuma cancanci yabo;
tilas a ji tsoronsa fiye da dukan alloli.
5 Gama dukan allolin al’ummai gumaka ne,
amma UBANGIJI ne ya yi sammai.
6 Daraja da ɗaukaka suna a gabansa;
ƙarfi da ɗaukaka suna a cikin tsarkakar wurinsa.

7 Ku ba wa UBANGIJI, ya iyalan al’ummai
ku ba wa UBANGIJI ɗaukaka da kuma ƙarfi.
8 Ku ba wa UBANGIJI ɗaukakar da ta dace da sunansa;
ku kawo sadaka ku kuma zo cikin filayen gidansa.
9 Ku bauta wa UBANGIJI da darajar tsarkinsa;
ku yi rawar jiki a gabansa, dukan duniya.
10 Ku faɗa cikin al’ummai, “UBANGIJI yana mulki.”
Duniya ta kahu daram, ba za a iya matsar da ita ba;
zai yi wa mutane hukunci da gaskiya.

11 Bari sammai su yi farin ciki, bari duniya tă yi murna;
bari teku tă yi ruri, da kuma dukan abin da yake cikinsa;
12 bari gonaki su yi tsalle da murna, da kuma kome da yake cikinsu.
Ta haka dukan itatuwan kurmi za su rera don farin ciki;
13 za su rera a gaban UBANGIJI, gama yana zuwa,
yana zuwa don yă hukunta duniya.
Zai hukunta duniya cikin adalci
mutane kuma cikin amincinsa.

# Zabura 97

1 UBANGIJI yana mulki, bari duniya tă yi murna;
bari tsibirai masu nesa su yi farin ciki.
2 Gizagizai da baƙin duhu sun kewaye shi;

* **Zabura 95:8** Meriba yana nufin faɗa. † **Zabura 95:8** Massa yana nufin gwaji.

adalci da gaskiya su ne tushen kursiyinsa.
3 Wuta tana tafiya a gabansa
tana kuma cinye maƙiyansa a kowane gefe.
4 Walƙiyarsa ta haskaka duniya;
duniya ta gani ta kuma yi rawar jiki.
5 Duwatsu sun narke kamar kakin zuma a gaban UBANGIJI,
a gaban Ubangijin dukan duniya.
6 Sammai sun yi shelar adalcinsa,
dukan mutane kuma suka ga ɗaukakarsa.

7 Dukan waɗanda suke bauta wa siffofi sun sha kunya,
waɗanda suke fariya da gumaka,
ku yi masa sujada, dukanku alloli!

8 Sihiyona ta ji ta kuma yi farin ciki
kuma dukan ƙauyukan Yahuda suna murna
saboda hukunce-hukuncenka, ya UBANGIJI.
9 Gama kai, ya UBANGIJI, kai ne Mafi Ɗaukaka a bisa dukan duniya;
ana darjanta ka fiye da dukan alloli.
10 Bari masu ƙaunar UBANGIJI su ƙi mugunta,
gama yana tsaron rayukan amintattunsa
yana kuma kuɓutar da su daga hannun mugaye.
11 An haskaka haske a kan masu adalci
da kuma farin ciki a kan masu gaskiya a zuciya.
12 Ku yi farin ciki a cikin UBANGIJI, ku da kuke masu adalci,
ku kuma yabi sunansa mai tsarki.

# Zabura 98

Zabura ce.
1 Ku rera sabuwar waƙa ga UBANGIJI,
gama ya yi abubuwa masu banmamaki;
hannunsa na dama da hannunsa mai tsarki
sun yi masa aikin ceto.
2 UBANGIJI ya sanar da cetonsa
ya kuma bayyana adalcinsa ga al'ummai.
3 Ya tuna da ƙaunarsa
da kuma amincinsa ga gidan Isra'ila;
dukan iyakar duniya sun ga
ceton Allahnmu.

4 Ku yi sowa don farin ciki ga UBANGIJI, dukan duniya,
ku ɓarke da waƙa ta murna tare da kiɗi;
5 ku yi kiɗi ga UBANGIJI da garaya,
da garaya da ƙarar rerawa,
6 tare da bushe-bushe da karar ƙahon rago,
ku yi sowa don farin ciki a gaban UBANGIJI, Sarki.

7 Bari teku su yi ruri, da kuma kome da yake cikinsa,
duniya da kuma kome da yake cikinta.
8 Bari koguna su tafa hannuwansu,
bari duwatsu su rera tare don farin ciki;

9 bari su rera a gaban UBANGIJI,
gama yana zuwa domin yǎ hukunta duniya.
Zai hukunta duniya da adalci
mutane kuma cikin gaskiya.

# Zabura 99

1 UBANGIJI yana mulki,
bari al’ummai su yi rawan jiki;
yana zaune a kursiyi tsakanin kerubobi,
bari duniya ta girgiza.
2 UBANGIJI mai girma yana a Sihiyona;
an ɗaukaka shi a bisa dukan al’ummai.
3 Bari mu yabi girmanka da sunanka mai banrazana,
shi mai tsarki ne.

4 Sarki mai iko ne, yana ƙaunar adalci
ka kafa gaskiya;
a cikin Yaƙub ka yi
abin da yake mai adalci da kuma daidai.
5 Ku ɗaukaka UBANGIJI Allahnmu
ku kuma yi masa sujada a wurin sa ƙafafunsa;
shi mai tsarki ne.

6 Musa da Haruna suna cikin firistocinsa,
Sama’ila yana cikin waɗanda suka kira bisa sunansa;
sun kira ga UBANGIJI
ya kuwa amsa musu.
7 Ya yi magana da su daga ginshiƙin girgije;
ya kiyaye farillansa da ƙa’idodin da ya ba su.

8 Ya UBANGIJI Allahnmu,
ka amsa musu;
ka kasance wa Isra’ila Allah mai gafartawa,
ko da yake ka hukunta ayyukansu marasa kyau.
9 Ku ɗaukaka UBANGIJI Allahnmu
ku kuma yi sujada a dutsensa mai tsarki,
gama UBANGIJI Allahnmu mai tsarki ne.

# Zabura 100

Zabura ce. Don yin godiya.
1 Ku yi sowa don farin ciki ga UBANGIJI, dukan duniya.
2 Yi wa UBANGIJI sujada da murna;
ku zo gabansa da waƙoƙin farin ciki.
3 Ku san cewa UBANGIJI shi ne Allah.
Shi ne ya yi mu, mu kuwa nasa ne;
mu mutanensa ne, tumakin makiyayarsa.

4 Ku shiga ƙofofinsa da godiya
filayen gidansa kuma da yabo;
ku gode masa ku kuma yabi sunansa.
5 Gama UBANGIJI yana da kyau kuma ƙaunarsa madawwamiya ce har abada;

amincinsa na cin gaba a dukan zamanai.

# Zabura 101

Ta Dawuda. Zabura ce.
1 Zan rera wa ƙauna da adalcinka;
gare ka, ya UBANGIJI, zan rera yabo.
2 Zan yi hankali ga yin rayuwa marar zargi,
yaushe za ka zo gare ni?

Zan bi da sha'anin gidana
da zuciya marar abin zargi
3 Ba zan kafa a gaban idanuna 1
wani abu marar kyau ba.

Na ƙi jinin ayyukan mutane marasa aminci;
ba za su manne mini ba.
4 Mutane masu mugun zuciya za su nesa da ni;
ba abin da zai haɗa ni da mugunta.

5 Duk wanda ya yi ɓatanci wa maƙwabcinsa a ɓoye
shi za a kashe;
duk mai renin wayo da mai girman kai,
ba zan jure masa ba.

6 Idanuna za su kasance a kan amintattu a cikin ƙasar,
don su zauna tare da ni;
tafiyarsa ba ta da zargi
zai yi mini hidima.

7 Babu mai ruɗun
da zai zauna a gidana;
babu mai ƙaryan
da zai tsaya a gabana.

8 Kowace safiya zan rufe bakunan
dukan mugaye a ƙasar;
zan yanke kowane mai aikata mugunta
daga birnin UBANGIJI.

# Zabura 102

Addu'ar mutum mai shan wahala. Sa'ad da ya rasa ƙarfi ya kuma yi makoki a gaban UBANGIJI.
1 Ka ji addu'ata, ya UBANGIJI;
bari kukata ta neman taimako ta zo gare ka.
2 Kada ka ɓoye fuskarka daga gare ni
sa'ad da nake cikin damuwa.
Ka juye kunnenka gare ni;
sa'ad da na yi kira, ka amsa mini da sauri.

3 Gama kwanakina sun ɓace kamar hayaƙi;
ƙasusuwana suna ƙuna kamar jan wuta.
4 Zuciyata ta kamu da ciwo ta kuma bushe kamar ciyawa;

na manta in ci abinci.
5 Saboda nishina mai ƙarfi
na rame na bar ƙasusuwa kawai.
6 Ni kamar mujiyar jeji ne,
kamar mujiya a kufai.
7 Na kwanta a faɗake; na zama
kamar tsuntsun da yake shi kaɗai a kan rufin ɗaki.
8 Dukan yini abokan gābana suna tsokanata;
waɗanda suke mini ba’a suna amfani da sunana yă zama abin la’ana.
9 Gama ina cin toka a matsayin abincina
ina kuma gauraye abin sha nawa da hawaye
10 saboda fushinka mai girma,
gama ka ɗaga ni sama ka yar a gefe.
11 Kwanakina suna kamar inuwar yamma;
na bushe kamar ciyawa.

12 Amma kai, ya Ubangiji, kana zaune a kursiyinka har abada;
sunan da ka yi zai dawwama a dukan zamanai.
13 Za ka tashi ka kuma ji tausayin Sihiyona,
gama lokaci ne na nuna alheri gare ta;
ƙayyadadden lokacin ya zo.
14 Gama duwatsunta suna da daraja ga bayinka;
ƙurarta kawai kan sa su ji tausayi.
15 Al’ummai za su ji tsoron sunan Ubangiji,
dukan sarakunan duniya za su girmama ɗaukakarka.
16 Gama Ubangiji zai sāke gina Sihiyona
ya kuma bayyana a ɗaukakarsa.
17 Zai amsa addu’ar marasa ƙarfi;
ba zai ƙyale roƙonsu ba.

18 Bari a rubuta wannan don tsara mai zuwa,
cewa mutanen da ba a riga an halitta ba za su yabi Ubangiji,
19 “Ubangiji ya duba ƙasa daga wurinsa mai tsarki a bisa,
daga sama ya hangi duniya,
20 don yă ji nishe-nishen ’yan kurkuku
yă kuma saki waɗanda aka yanke musu hukuncin mutuwa.”
21 Saboda haka za a furta sunan Ubangiji a Sihiyona
yabonsa kuma a Urushalima
22 sa’ad da mutane da mulkoki
suka tattaru don su yi wa Ubangiji sujada.

23 Cikin rayuwata, ya karye ƙarfina;
ya gajartar da kwanakina.
24 Sai na ce,
“Kada ka ɗauke ni a tsakiyar kwanakina, ya Allah;
shekarunka suna bi cikin dukan zamanai.
25 A farkon fari ka kafa tushen duniya,
sammai kuma aikin hannuwanka ne.
26 Za su hallaka, amma za ka ci gaba;
duk za su tsufe kamar riga.
Kamar riga za ka canja su

za a kuwa zubar da su.
27 Amma kana nan yadda kake,
kuma shekarunka ba za su taɓa ƙarewa ba.
28 'Ya'yan bayinka za su zauna a gabanka;
zuriyarsu za su kahu a gabanka."

# Zabura 103

Ta Dawuda.
1 Yabi UBANGIJI, ya raina;
dukan abin da yake cikin cikina, yabi sunansa mai tsarki.
2 Yabi UBANGIJI, ya raina,
kada kuma ka manta dukan alheransa,
3 wanda yake gafarta dukan zunubai
yake kuma warkar da dukan cututtuka,
4 wanda ya fanshi ranka daga rami
ya naɗa maka rawani da ƙauna da kuma tausayi,
5 Wanda ya ƙosar da kai da abubuwa masu kyau
domin a sabunta ƙuruciyarka kamar na gaggafa.

6 UBANGIJI yana aikata adalci
da kuma gaskiya ga duk waɗanda aka danne.

7 Ya sanar da hanyoyinsa wa Musa,
ayyukansa ga mutanen Isra'ila.
8 UBANGIJI mai tausayi ne da kuma alheri,
mai jinkirin fushi, cike da ƙauna.
9 Ba zai yi ta zargi ba
ba kuwa zai yi ta jin fushi har abada ba;
10 ba ya yin da mu gwargwadon zunubanmu
ko yǎ sāka mana bisa ga laifofinmu.
11 Gama kamar yadda sammai suke can bisa duniya,
haka girmar ƙaunarsa yake wa masu tsoronsa;
12 kamar yadda gabas yake daga yamma,
haka ya cire laifofinmu daga gare mu.

13 Kamar yadda mahaifi yake jin tausayin 'ya'yansa,
haka UBANGIJI yake jin tausayin waɗanda suke tsoronsa;
14 gama ya san yadda aka yi mu,
ya tuna cewa mu ƙura ne.
15 Game da mutum dai, kwanakinsa suna kamar ciyawa
da suke haɓaka kamar fure a gona;
16 iska kan hura a kansa sai ya ɓace
ba a kuwa sāke tuna da inda dā yake.
17 Amma daga madawwami zuwa madawwami
ƙaunar UBANGIJI tana tare da waɗanda suke tsoronsa,
adalcinsa kuma tare da 'ya'yansu,
18 tare da waɗanda suke kiyaye alkawarinsa
suna kuma tuna su yi biyayya da farillansa.

19 UBANGIJI ya kafa kursiyinsa a sama,
masarautarsa kuwa na mulki a bisa duka.

20 Yabi UBANGIJI, ku mala'ikunsa,
ku jarumawa masu yi masa aiki,
waɗanda suke yin biyayya da maganarsa.
21 Yabi UBANGIJI, dukanku rundunarsa ta sama,
ku bayinsa waɗanda kuke aikata nufinsa.
22 Yabi UBANGIJI, dukanku ayyukansa
ko'ina a mulkinsa.

Yabi UBANGIJI, ya raina.

# Zabura 104

1 Yabi UBANGIJI, ya raina.

Ya UBANGIJI Allahna, kana da girma ƙwarai;
kana saye da daraja da ɗaukaka.

2 UBANGIJI ya naɗe kansa da haske kamar riga
ya shimfiɗa sammai kamar tenti
3 ya kafa ginshiƙan ɗakin samansa a kan ruwaye.
Ya maido da gizagizai suka zama keken yaƙinsa
yana hawa a kan fikafikan iska.
4 Ya mai da iska suka zama 'yan saƙonsa
harsunan wuta kuma bayinsa.

5 Ya kafa duniya a kan tussanta;
ba za a iya matsar da ita ba.
6 Ka rufe ta da zurfi kamar da riga
ruwaye sun tsaya a bisa duwatsu.
7 Amma a tsawatawarka ruwaye suka gudu
da jin ƙarar tsawanka suka ruga da gudu;
8 suka gudu a bisa duwatsu,
suka gangara zuwa cikin kwaruruka,
zuwa wurin da ka shirya musu.
9 Ka kafa iyakar da ba a iya tsallakawa;
ba za su ƙara rufe duniya ba.

10 Ya sa maɓulɓulai suka zuba ruwa cikin kwaruruka;
yana gudu tsakanin duwatsu.
11 Suna ba da ruwa ga dukan namun jeji;
jakunan jeji suna kashe ƙishirwansu.
12 Tsuntsaye sarari suna sheƙunansu kusa da ruwan;
suna rera cikin rassa.
13 Yana wa duwatsu banruwa daga ɗakinsa na sama;
ƙasa tana ƙoshiya da amfanin aikinsa.
14 Yana sa ciyawa tă yi girma saboda shanu,
tsire-tsire domin mutum ya nome,
suna fid da abinci daga ƙasa,
15 ruwan inabi yakan sa zuciyar mutum tă yi murna,
mai kuwa yakan sa fuska tă yi haske,
abinci kuma da yake riƙe zuciyarsa.
16 Ana yi wa itatuwan UBANGIJI banruwa sosai,

al’ul na Lebanon da ya shuka.
17 A can tsuntsaye suke sheƙunnansu;
shamuwa tana da gidanta a itatuwan fir.
18 Manyan duwatsu na awakin jeji ne;
tsagaggun duwatsun mafaka ne ga rema.

19 Wata ne ke ƙididdigar lokuta,
rana kuma ta san sa’ad da za tă fāɗi.
20 Ka yi duhu, sai ya zama dare,
sai dukan namun jeji a kurmi suka fito a maƙe.
21 Zakoki sun yi ruri sa’ad da suke farauta
suna kuma neman abincinsu daga Allah.
22 Rana ta fito, sai suka koma shiru;
suka koma suka kwanta a kogwanninsu.
23 Mutum yakan tafi aikinsa,
zuwa wurin aikinsa har yamma.

24 Ina misalin yawan aikinka, ya UBANGIJI!
Cikin hikima ka yi su duka;
duniya ta cika da halittunka.
25 Akwai teku, babba da kuma fāɗi,
cike da halittun da suka wuce ƙirga,
abubuwa masu rai babba da ƙarami.
26 A can jiragen ruwa suna kai komo,
kuma dodon ruwan da ka yi, yă yi wasa a can.

27 Waɗannan duka suna dogara gare ka
don ka ba su abincinsu a daidai lokaci.
28 Sa’ad da ba su da shi,
sai su tattara shi;
sa’ad da ka buɗe hannunka,
sukan ƙoshi da abubuwa masu kyau.
29 Sa’ad da ka ɓoye fuskarka,
sai su razana;
sa’ad da ka ɗauke numfashinsu,
sai su mutu su kuma koma ga ƙura.
30 Sa’ad da ka aika da Ruhunka,
sai su halittu,
su kuma sabunta fuskar duniya.

31 Bari ɗaukakar UBANGIJI ta dawwama har abada;
bari UBANGIJI yă yi farin ciki cikin aikinsa,
32 shi wanda ya dubi duniya, sai ta razana,
wanda ya taɓa duwatsu, sai suka yi hayaƙi.

33 Zan rera ga UBANGIJI dukan raina;
zan rera yabo ga Allahna muddin ina raye.
34 Bari tunanina yă gamshe shi,
yayinda nake farin ciki a cikin UBANGIJI.
35 Amma bari masu zunubi su ɓace daga duniya
mugaye kuma kada a ƙara ganinsu.

Yabi UBANGIJI, ya raina.

Yabi UBANGIJI.*

# Zabura 105

1 Ku yi godiya ga UBANGIJI, ku kira bisa sunansa;
ku sanar a cikin al'ummai abin da ya yi.
2 Ku rera gare shi, ku rera yabo gare shi;
ku faɗa dukan abubuwan mamakin da ya aikata.
3 Ku ɗaukaka a cikin sunansa mai tsarki;
bari zukatan waɗanda suke neman UBANGIJI su yi farin ciki.
4 Ku sa rai ga UBANGIJI da kuma ƙarfinsa;
ku nemi fuskarsa kullum.

5 Ku tuna da abubuwan mamakin da ya yi,
mu'ujizansa, da kuma hukunce-hukuncen da ya zartar,
6 Ya ku zuriyar Ibrahim bawansa,
Ya ku 'ya'yan Yaƙub, zaɓaɓɓensa.
7 Shi ne UBANGIJI Allahnmu;
kuma hukunce-hukuncensa suna a cikin dukan duniya.

8 Yana tuna da alkawarinsa har abada,
maganar da ya umarta, har tsararraki dubu,
9 alkawarin da ya yi da Ibrahim,
rantsuwar da ya yi wa Ishaku.
10 Ya tabbatar da shi ga Yaƙub a matsayin ƙa'ida,
Isra'ila a matsayin madawwamin alkawari,
11 "Gare ka zan ba da ƙasar Kan'ana
a matsayin rabo za ka yi gādo."

12 Sa'ad da suke kima kawai,
kima sosai, da kuma baƙi a cikinta,
13 suka yi ta yawo daga al'umma zuwa al'umma,
daga masarauta zuwa wata.
14 Bai bar kowa yă danne su ba;
saboda su, ya tsawata wa sarakuna,
15 "Kada ku taɓa shafaffena;
kada ku yi wa annabawa lahani."

16 Ya sauko da yunwa a kan ƙasa
ya kuma lalace dukan tanadinsu na abinci;
17 ya kuma aiki mutum a gabansu,
Yusuf, da aka sayar a matsayin bawa.
18 Suka raunana ƙafafunsa da sarƙa
aka sa wuyansa cikin ƙarafa,
19 sai abin da ya rigafaɗi ya cika
sai da maganar UBANGIJI ta tabbatar da shi mai gaskiya.
20 Sarki ya aika aka kuma sake shi,
mai mulkin mutane ya 'yantar da shi.

* **Zabura 104:35** Da Ibraniyanci Hallelu Ya; a cikin Seftuwajin wannan layi yana a farkon Zabura 105.1.

21 Ya mai da shi shugaban gidansa,
mai mulki a bisa dukan abin da ya mallaka,
22 don yă umarci sarakunansa yadda ya ga dama
yă kuma koya wa dattawa hikima.

23 Sa'an nan Isra'ila ya shiga Masar;
Yaƙub ya yi zama kamar baƙo a ƙasar Ham.
24 UBANGIJI ya mai da mutanensa suka yi ta haihuwa;
ya sa suka yi yawa suka fi ƙarfin maƙiyansu,
25 waɗanda ya juya zukatansu su ƙi mutanensa
don su haɗa baki a kan bayinsa.
26 Ya aiki Musa bawansa,
da Haruna, wanda ya zaɓa.
27 Suka yi mu'ujizansa a cikinsu,
abubuwan mamakinsa a cikin ƙasar Ham.
28 Ya aiko da duhu ya kuma sa ƙasar tă yi duhu,
ba domin sun yi tawaye a kan maganarsa ba?
29 Ya mai da ruwaye suka zama jini,
ya sa kifayensu suka mutu.
30 Kasarsu ta yi ta fid da kwaɗi,
waɗanda suka haura cikin ɗakunan kwana na masu mulkinsu.
31 Ya yi magana, sai tarin ƙudaje suka fito,
cinnaku kuma ko'ina a ƙasar.
32 Ya mai da ruwan samansu ya zama ƙanƙara,
da walƙiya ko'ina a ƙasarsu;
33 ya lalace inabinsu da itatuwan ɓaurensu
ya ragargaza itatuwan ƙasarsu.
34 Ya yi magana, sai fāri ɗango suka fito,
fāran da ba su ƙidayuwa;
35 suka cinye kowane abu mai ruwan kore a cikin ƙasarsu,
suka cinye amfanin gonarsu
36 Sa'an nan ya karkashe dukan 'yan fari a cikin ƙasarsu,
nunan fari na dukan mazantakarsu.
37 Ya fitar da Isra'ila, ɗauke da azurfa da zinariya,
kuma daga cikin kabilansu babu wani da ya kāsa.
38 Masar ta yi murna sa'ad da suka tafi,
saboda tsoron Isra'ila ya fāɗo musu.

39 Ya shimfiɗa girgije kamar mayafi,
da kuma wuta don ta ba su haske da dare.
40 Suka roƙa, ya kuwa ba su makware
ya kuma ƙosar da su da abinci daga sama.
41 Ya buɗe dutse, sai ruwa ya ɓulɓulo,
kamar kogi ya gudu zuwa cikin hamada.

42 Ya tuna da alkawarinsa mai tsarki
da ya ba wa bawansa Ibrahim.
43 Ya fitar da mutanensa da farin ciki,
zaɓaɓɓunsa da sowa ta farin ciki;
44 ya ba su ƙasashen al'ummai,
suka kuma sami gādon abin da waɗansu sun sha wahala a kai,

45 don su kiyaye farillansa
su kuma kiyaye dokokinsa.

Yabo ga UBANGIJI.*

# Zabura 106

1 Yabi UBANGIJI.*

Yi godiya ga UBANGIJI, gama nagari ne shi;
ƙaunarsa madawwamiya ce har abada.

2 Wane ne zai furta manyan ayyukan UBANGIJI
ko yă furta cikakken yabonsa?
3 Masu albarka ne waɗanda suke yin adalci,
waɗanda kullum suke yin abin da yake daidai.

4 Ka tuna da ni, ya UBANGIJI, sa'ad da ka nuna alheri ga mutanenka,
ka zo ka taimake ni sa'ad da ka cece su,
5 don in ji daɗin nasarar zaɓaɓɓunka,
don in sami rabo cikin farin cikin al'ummarka
in kuma shiga gādonka cikin yin yabo.

6 Mun yi zunubi, kamar yadda kakanninmu suka yi;
mun yi ba daidai ba muka kuma aikata mugunta.
7 Sa'ad da kakanninmu suke a Masar,
ba su damu da mu'ujizanka ba;
ba su tuna yawan alheranka ba,
suka kuma yi tayarwa a teku, Jan Teku.
8 Duk da haka ya cece su saboda sunansa,
don yă sanar da ikonsa mai girma.
9 Ya tsawata wa Jan Teku, ya kuwa bushe;
ya bi da su ta cikin zurfafa sai ka ce a hamada.
10 Ya cece su daga hannun maƙiyi;
daga hannun abokin gāba ya fanshe su.
11 Ruwaye suka rufe abokan gābansu;
babu ko ɗaya da ya tsira.
12 Sa'an nan suka gaskata alkawarinsa
suka kuma rera yabonsa.

13 Amma nan da nan suka manta abin da ya yi
ba su kuwa jira shawararsa ba.
14 A cikin hamada suka bar sha'awarsu ta mamaye su
a ƙasar da babu kome suka gwada Allah.
15 Sai ya ba su abin da suka roƙa,
amma ya aika musu da muguwar cuta.

16 A sansani suka ji kishin Musa
da kuma Haruna, wanda UBANGIJI ya keɓe.
17 Kasa ta buɗe ta haɗiye Datan

* **Zabura 105:45** Da Ibraniyanci Hallelu Ya * **Zabura 106:1** Da Ibraniyanci Hallelu Ya; haka kuma a aya 48.

ta binne iyalin Abiram.
18 Wuta ta ƙuno a cikin mabiyansu;
harshen wuta ya cinye mugaye.
19 A Horeb suka yi ɗan maraƙi
suka yi wa gunkin zubi daga ƙarfe sujada.
20 Suka sauke Ɗaukakarsu
saboda siffar bijimi, wanda yake cin ciyawa.
21 Suka manta da Allahn da ya cece su,
wanda ya aikata manyan abubuwa a Masar,
22 mu'ujizai a ƙasar Ham
ayyukan banrazana a Jan Teku.
23 Don haka ya ce zai hallaka su,
amma Musa, zaɓaɓɓensa,
ya yi godo a gabansa
don yǎ kau da hasalarsa daga hallaka su.

24 Sai suka rena ƙasa mai ni'ima;
ba su gaskata alkawarinsa ba.
25 Suka yi gunaguni a tentunansu
ba su kuwa yi biyayya da Ubangiji ba.
26 Saboda haka ya rantse musu ya kuma ɗaga hannu
cewa zai sa su mutu a cikin hamada,
27 ya sa zuriyarsu su mutu a cikin al'ummai
ya kuma watsar da su cikin dukan ƙasashe.

28 Suka haɗa kai da Ba'al-Feyor
suka kuma ci hadayun da aka miƙa wa allolin da ba su da rai;
29 suka tsokane Ubangiji ya yi fushi ta wurin mugayen ayyukansu,
sai annoba ta ɓarke a cikinsu.
30 Amma Finehas ya miƙe tsaye ya ɗauki mataki,
sai annobar ta daina.
31 An ayana masa wannan a matsayin adalci
har zamanai marar matuƙa masu zuwa.
32 A ruwan Meriba suka ba Ubangiji fushi,
sai wahala ta zo wa Musa saboda su;
33 saboda sun yi tayarwa a kan Ruhun Allah,
har mugayen kalmomi suka fito daga leɓunan Musa.

34 Ba su hallakar da mutanen
yadda Ubangiji ya umarce su ba,
35 amma suka yi cuɗanya da al'ummai
suka ɗauki al'adunsu.
36 Suka yi wa gumakansu sujada,
waɗanda suka zama tarko gare su.
37 Suka miƙa 'ya'yansu maza hadaya
'yan matansu kuma ga aljanu.
38 Suka zub da jini marar laifi,
jinin 'ya'yansu maza da mata,
waɗanda suka miƙa hadaya ga gumakan Kan'ana,
ƙasar kuwa ta ƙazantu ta wurin jininsu.
39 Suka ƙazantar da kansu ta wurin abin da suka yi;

ta wurin ayyukansu suka yi karuwanci.

40 Saboda haka UBANGIJI ya yi fushi da mutanensa
ya ji ƙyamar gādonsa.
41 Ya miƙa su ga al'ummai,
maƙiyansu kuma suka yi mulki a kansu.
42 Abokan gābansu suka danne su
suka sa su a ƙarƙashin ikonsu.
43 Sau da yawa ya cece su,
amma sun nace su yi tawaye
suka kuma lalace cikin zunubinsu.
44 Amma ya lura da wahalarsu
sa'ad da ya ji kukansu;
45 saboda su ya tuna da alkawarinsa
kuma daga yawan ƙaunarsa ya ji tausayi.
46 Ya sa aka ji tausayinsu
a wurin dukan waɗanda suka kame su.

47 Ka cece mu, UBANGIJI Allahnmu,
ka kuma tattara mu daga al'ummai,
don mu yi wa sunanka mai tsarki godiya
mu kuma ɗaukaka cikin yabonka.

48 Yabo ga UBANGIJI, Allah na Isra'ila,
daga madawwami zuwa madawwami.

Bari dukan mutane su ce, "Amin!"

Yabo ga UBANGIJI.

# LITTAFI NA BIYAR

## 107

*Zabura 107–150*

1 Ku yi godiya ga UBANGIJI, gama nagari ne shi;
ƙaunarsa madawwamiya ce har abada.

2 Bari fansassu na UBANGIJI su faɗa wannan,
su da aka fansa daga hannun maƙiyi,
3 su da ya tattara daga ƙasashe,
daga gabas da yamma, daga arewa da kudu.

4 Waɗansu sun yi ta yawo a jejin hamada,
ba su sami hanya zuwa birnin da za su zauna ba.
5 Sun ji yunwa da ƙishirwa,
suka kuma fid da zuciya.
6 Sa'an nan suka yi kuka ga UBANGIJI cikin wahalarsu,
ya kuma cece su daga damuwarsu.
7 Ya bishe su ta miƙaƙƙiyar hanya
zuwa birnin da za su zauna.
8 Bari su yi godiya ga UBANGIJI saboda ƙaunarsa marar ƙarewa
da kuma ayyukansa masu banmamaki saboda mutane,

9 gama yana shayar da masu ƙishirwa
yana kuma ƙosar da mayunwata da abubuwa masu kyau.

10 Waɗansu sun zauna a cikin duhu da kuma zurfin ɓacin rai,
'yan kurkuku suna wahala cikin sarƙoƙin ƙarfe,
11 gama sun yi tayarwa a kan maganar Allah
suka ƙi shawarar Mafi Ɗaukaka.
12 Saboda haka ya ba da su ga aiki mai wuya;
suka yi tuntuɓe, kuma ba mai taimako.
13 Sa'an nan suka yi kuka ga UBANGIJI cikin wahalarsu,
ya kuwa cece su daga damuwarsu.
14 Ya fitar da su daga duhu da zurfin ɓaci rai
ya tsintsinke sarƙoƙinsu.
15 Bari su yi godiya ga UBANGIJI saboda ƙaunarsa marar ƙarewa
da kuma ayyukansa masu banmamaki saboda mutane,
16 gama ya farfashe ƙofofin tagulla
ya kuma ragargaza ƙyamaren ƙarfe.

17 Waɗansu suka zama wawaye ta wurin hanyoyinsu na tayarwa
suka kuwa sha wahala saboda laifofinsu.
18 Ba su so su ga abinci ba
suka kuwa kai bakin mutuwa.
19 Sa'an nan suka yi kuka ga UBANGIJI cikin wahalarsu,
ya kuwa cece su daga damuwarsu.
20 Ya ba da umarninsa ya kuma warkar da su
ya kuɓutar da su daga kabari.
21 Bari su yi godiya ga UBANGIJI saboda ƙaunarsa marar ƙarewa
da kuma ayyukansa masu banmamaki saboda mutane.
22 Bari su miƙa hadaya ta godiya
su kuma ba da labarin ayyukansa da waƙoƙin farin ciki.

23 Waɗansu suka yi tafiya a teku cikin jiragen ruwa;
su 'yan kasuwa ne a manyan ruwaye.
24 Sun ga ayyukan UBANGIJI,
ayyukansa masu banmamaki a cikin zurfin teku.
25 Gama ya yi magana ya kuma sa iska mai ƙarfi ta tashi
ya ɗaga raƙuman ruwa sama.
26 Suka hau zuwa sammai suka kuma tsinduma cikin zurfafa;
a cikin azabarsu sai ƙarfin halinsu ya karai.
27 Suka yi tangaɗi suna tuntuɓe kamar bugaggu;
suka kuma kai ga ƙarshen dabararsu.
28 Sai suka yi kuka ga UBANGIJI cikin wahalarsu,
ya kuwa fitar da su daga damuwarsu.
29 Ya kwantar da hadiri suka yi tsit;
raƙuman ruwan teku suka yi shiru.
30 Suka yi murna sa'ad da wuri ya kwanta,
ya kuma bishe su zuwa inda suka so su kai.
31 Bari su yi godiya ga UBANGIJI saboda ƙaunarsa marar ƙarewa
da kuma ayyukansa masu banmamaki saboda mutane.
32 Bari su ɗaukaka shi cikin taron mutane
su kuma yabe shi cikin taron dattawa.

33 Ya mai da koguna suka zama hamada,
maɓulɓulai masu gudu suka zama ƙasa mai ƙishirwa,
34 ƙasa mai amfani kuma suka zama gishiri marar amfani,
saboda muguntar waɗanda suka zauna a can.
35 Ya mai da hamada ya zama tafkunan ruwa
busasshiyar ƙasa kuma zuwa maɓulɓulai masu gudu;
36 a can ya kai mayunwata su yi zama,
ya kuma samo birnin da za su zauna.
37 Suka yi shuka a gonaki suka dasa inabi
suka kuma girbe amfani gona;
38 ya albarkace su, yawansu kuma ya ƙaru,
bai kuwa bar garkunansu suka ragu ba.

39 Sa'an nan yawansu ya ragu, aka kuma ƙasƙantar da su
ta wurin danniya, bala'i da kuma baƙin ciki;
40 shi da yake kawo reni a kan manyan mutane
ya sa suka yi ta yawo a cikin jejin da ba hanya.
41 Amma ya fid da mabukata daga wahalarsu
ya kuma ƙara iyalansu da tumakinsu.
42 Masu yin gaskiya suka gani suka yi farin ciki
amma dukan mugaye suka rufe bakunansu.

43 Duk mai hikima, bari yă ji waɗannan abubuwa
yă kuma lura da ƙauna mai girma ta UBANGIJI.

# Zabura 108

Waƙa ce. Zabura ta Dawuda.
1 Zuciyata tsayayyiya ce, ya Allah;
zan rera in kuma yi kiɗi da dukan raina.
2 Ku farka, garaya da molo!
Zan farkar da rana.
3 Zan yabe ka, ya UBANGIJI, a cikin al'ummai;
zan rera game da kai cikin mutane.
4 Gama ƙaunarka da girma take, bisa fiye da sammai;
amincinka ya kai sarari.
5 A ɗaukaka ka, ya Allah, a bisa sammai,
bari kuma ɗaukakarka ta kasance a bisa dukan duniya.

6 Ka cece mu ka kuma taimake mu da hannunka na dama,
domin waɗanda kake ƙauna su kuɓuta.
7 Allah ya yi magana daga wurinsa mai tsarki,
"Ciki nasara zan raba Shekem
in kuma auna Kwarin Sukkot.
8 Gileyad nawa ne, Manasse nawa ne;
Efraim shi hulan kwanona,
Yahuda ne sandana na sarauta.
9 Mowab shi ne kwanon wankina,
a kan Edom zan jefa takalmina;
a bisa Filistiya zan yi kirari cikin nasara."

10 Wa zai kawo ni birni mai katanga?
Wa zai jagorance ni zuwa Edom?

11 Ba kai ba ne, ya Allah, kai da ka ƙi mu
ba ka kuwa fita tare da mayaƙanmu?
12 Ka ba mu taimako a kan abokin gāba,
gama taimakon mutum banza ne.
13 Tare da Allah za mu yi nasara,
zai kuma tattaka abokan gābanmu.

# Zabura 109

Don mai bi da kaɗe-kaɗe. Ta Dawuda. Zabura ce.
1 Ya Allah, wanda nake yabo,
kada ka yi shiru,
2 gama mugaye da masu ruɗu
sun buɗe bakunansu a kaina;
sun yi magana a kaina da harsunan ƙarya.
3 Da kalmomin ƙiyayya sun kewaye ni;
sun tasar mini ba dalili.
4 A maimakon ƙauna sun sāka mini da zargi,
amma ni mutum ne mai addu'a.
5 Sun sāka mini alheri da mugunta,
ƙauna kuma da ƙiyayya.

6 Ka naɗa mugun mutum yă yi hamayya da shi;
bari mai zargi yă tsaya a hannun damansa.
7 Sa'ad da aka yi masa shari'a, bari a same shi da laifi,
bari kuma addu'o'insa su hukunta shi.
8 Bari kwanakinsa su zama kaɗan;
bari wani yă ɗauki wurinsa na shugabanci.
9 Bari 'ya'yansa su zama marayu
matarsa kuma gwauruwa.
10 Bari 'ya'yansa su zama masu yawo suna bara;
bari a yi ta koransu daga gidajensu da suke kufai.
11 Bari mai binsa bashi yă ƙwace dukan abin da yake da shi;
bari baƙi su washe amfanin aikinsa.
12 Bari kada kowa yă yi masa alheri
ko yă ji tausayin marayunsa.
13 Bari duk zuriyarsa su mutu,
a shafe sunayensu daga tsara mai zuwa.
14 Bari a tuna da laifin kakanninsa a gaban UBANGIJI;
bari kada a taɓa shafe zunubin mahaifiyarsa.
15 Bari zunubansu su kasance a gaban UBANGIJI kullum,
don yă sa a manta da su daga duniya.

16 Gama bai taɓa yin tunanin yin alheri ba,
amma ya tsananta wa matalauta
da mabukata da kuma masu fid da zuciya har suka mutu.
17 Yana jin daɗin la'antarwa,
bari yă dawo a kansa;
ba ya son sa albarka,
bari kada kowa yă sa masa albarka.
18 Ya sa la'antarwa kamar rigarsa;
ta shiga cikin jikinsa kamar ruwa,

cikin ƙasusuwansa kamar mai.
19 Bari tă zama kamar mayafin da aka ɗaura kewaye da shi,
kamar ɗamara da aka ɗaura kewaye da shi har abada.
20 Bari wannan yă zama sakayyar UBANGIJI ga masu zargina,
ga waɗanda suke mugayen maganganu a kaina.

21 Amma kai, ya UBANGIJI Mai Iko Duka,
ka yi da ni da kyau saboda sunanka;
ta alherin ƙaunarka, ka cece ni.
22 Gama ni matalauci ne mai bukata kuma,
zuciyata kuwa ta yi rauni a cikina.
23 Na ɓace kamar inuwar yamma;
ana kakkaɓe ni kamar fāra.
24 Gwiwoyina suna mutuwa saboda azumi;
jikina ya rame ba kuma ƙarfi.
25 Na zama abin dariya ga masu zargina;
sa'ad da suka gan ni, suka kaɗa kawunansu.

26 Ka taimake ni, ya UBANGIJI Allahna;
ka cece ni bisa ga ƙaunarka.
27 Bari su san cewa hannunka ne,
cewa kai ne, ya UBANGIJI, ka yi shi.
28 Za su iya la'anta, amma kai za ka sa albarka;
sa'ad da suka tasar za su sha kunya,
amma bawanka zai yi farin ciki.
29 Masu zargina za su sha kunya
za a rufe su da kunya kamar mayafi.

30 Da bakina zan ɗaukaka UBANGIJI sosai;
cikin babban taro zan yabe shi.
31 Gama yana tsaya a hannun damar mai bukata,
don yă cece ransa daga waɗanda suke hukunta shi.

# Zabura 110

Ta Dawuda. Zabura ce.
1 UBANGIJI ya ce wa Ubangijina,
"Zauna a hannun damana,
sai na sa abokan gābanka
su zama matashin sawunka."

2 UBANGIJI zai fadada ikon sandan mulkinka daga Sihiyona
za ka yi mulki a tsakiyar abokan gābanka.
3 Rundunarka za su so yin yaƙi
a ranarka ta yaƙi.
Saye cikin ɗaukaka mai tsarki,
daga cikin ciki na safiya
za ka karɓi raɓar ƙuruciyarka.*

4 UBANGIJI ya rantse
ba zai kuma canja zuciyarsa ba,

* **Zabura 110:3** Ko kuwa / samarinka za su zo gare ka kamar raba

"Kai firist ne har abada,
bisa ga tsarin Melkizedek."

5 Ubangiji yana a hannun damanka;
zai murƙushe sarakuna a ranar fushinsa.
6 Zai hukunta al'ummai, yana tarawa gawawwaki
yana kuma murƙushe masu mulkin dukan duniya.
7 Zai sha daga rafin da yake kusa da hanya;
saboda haka zai ɗaga kansa sama.
*

# Zabura 111

1 Yabi UBANGIJI.†

Zan ɗaukaka UBANGIJI da dukan zuciyata
a cikin majalisar masu aikata gaskiya da kuma a cikin taro.

2 Ayyukan UBANGIJI da girma suke;
dukan waɗanda suke farin ciki da su suna tunaninsu.
3 Ayyukansa masu ɗaukaka da kuma daraja ne,
adalcinsa kuma zai dawwama har abada.
4 Ya sa a tuna da abubuwa masu banmamaki nasa;
UBANGIJI mai alheri ne mai tausayi kuma.
5 Yana ba da abinci ga waɗanda suke tsoronsa;
yakan tuna da alkawarinsa har abada.

6 Ya nuna wa mutanensa ikon ayyukansa,
yana ba su ƙasashen waɗansu al'ummai.
7 Ayyukan hannuwansa masu aminci ne da kuma gaskiya;
dukan farillansa abin dogara ne.
8 Tsayayyu ne har abada abadin,
ana yinsu cikin aminci da kuma gaskiya.
9 Yana ba da ceto ga mutanensa;
ya kafa alkawarinsa har abada,
tsarki da banrazana ne sunansa.

10 Tsoron UBANGIJI ne mafarin hikima;
dukan waɗanda suke bin farillansa suna da ganewa mai kyau.
Gare shi ne madawwamin yabo.
*

# Zabura 112

1 Yabi UBANGIJI.†

Mai albarka ne mutumin da yake tsoron UBANGIJI,
wanda yakan sami farin ciki mai girma a umarnansa.

2 'Ya'yansa za su zama manya a ƙasar;
tsaran masu aikata gaskiya za su sami albarka.

* **Zabura 111:** Wannan Zabura waƙa ce, layinta sun fara da jerin harufan Ibraniyanci bi da bi. † **Zabura 111:1** Da Ibraniyanci Hallelu Ya * **Zabura 112:** Wannan Zabura waƙa ce, layinta sun fara da jerin harufan Ibraniyanci bi da bi. † **Zabura 112:1** Da Ibraniyanci Hallelu Ya

3 Wadata da arziki suna a cikin gidansa,
adalcinsa zai dawwama har abada.
4 Ko a cikin duhu haske kan haskaka wa mai aikata gaskiya,
mai alheri mai tausayi da kuma mai adalci.‡
5 Abu mai kyau zai zo masa shi da yake kyauta yake kuma ba da bashi hannu sake,
shi da yake yin al'amuransa cikin gaskiya.

6 Tabbatacce ba zai taɓa jijjigu ba;
za a tuna da mai adalci har abada.
7 Ba zai ji tsoron labari marar daɗi ba;
zuciyarsa tsayayyiya ce, tana dogara ga UBANGIJI.
8 Zuciyarsa tana da kāriya, ba zai ji tsoro ba;
a ƙarshe zai zama mai nasara a kan maƙiyansa.
9 Ya rarraba kyautansa ga matalauta,
adalcinsa zai dawwama har abada;
za a ɗaga ƙahonsa§ sama da bangirma.

10 Mugun mutum zai gani yă kuma yi fushi,
zai ciza haƙora yă kuma lalace;
sha'awace-sha'awacen mugaye za su zo ga ƙarshe.

# Zabura 113

1 Yabi UBANGIJI.*

Ku yabe shi, ya ku bayin UBANGIJI,
ku yabi sunan UBANGIJI.
2 Bari a yabi sunan UBANGIJI,
yanzu da har abada kuma.
3 Daga fitowar rana zuwa inda take fāɗuwa,
a yabi sunan UBANGIJI.

4 Ana ɗaukaka UBANGIJI a bisa dukan al'ummai,
ɗaukakarsa a bisa sammai
5 Wane ne yake kamar UBANGIJI Allahnmu,
Wannan mai zama a kursiyi can bisa,
6 wanda yake sunkuya yă dubi
sammai da duniya?

7 Yakan tā da matalauta daga ƙura
yakan ɗaga mabukata daga tarin toka;
8 ya zaunar da su tare da sarakuna,
tare da sarakunan mutanensu.
9 Yakan zaunar da matar da ba haihuwa a gidanta
ta zama kamar mahaifiyar 'ya'ya mai farin ciki.

Yabi UBANGIJI.

# Zabura 114

1 Sa'ad da Isra'ila ya fito daga Masar,

---

‡ **Zabura 112:4** Ko kuwa / gama UBANGIJI mai alheri ne, mai tausayi da kuma mai adalci. § **Zabura 112:9** Kaho a nan yana nufin girma. * **Zabura 113:1** Da Ibraniyanci Hallelu Ya, haka ma a aya 9.

gidan Yaƙub daga mutane masu baƙon harshe,
2 Yahuda ya zama wuri mai tsarki na Allah,
Isra'ila mallakarsa.

3 Teku ya kalla ya kuma gudu,
Urdun ya juye da baya;
4 duwatsu suka yi tsalle kamar raguna,
tuddai kamar tumaki.

5 Me ya sa, ya teku, kika gudu,
Ya Urdun, ka juya baya,
6 ku duwatsu, kuka yi tsalle kamar raguna,
ku tuddai, kamar tumaki?

7 Ki yi rawar jiki, ya duniya, a gaban Ubangiji,
a gaban Allah na Yaƙub,
8 wanda ya juye dutse ya zama tafki,
dutse mai ƙarfi zuwa maɓulɓulan ruwa.

# Zabura 115

1 Ba gare mu ba, ya UBANGIJI, ba gare mu ba
amma ga sunanka yă sami ɗaukaka,
saboda ƙaunarka da amincinka.

2 Me ya sa al'ummai suke cewa,
"Ina Allahnsu?"
3 Allahnmu yana a sama;
yana yin duk abin da ya ga dama.
4 Amma gumakansu azurfa da zinariya ne,
da hannuwan mutane suka yi.
5 Suna da bakuna, amma ba sa magana,
idanu, amma ba sa gani;
6 suna da kunnuwa, amma ba sa ji,
hanci, amma ba sa jin ƙanshi
7 suna da hannuwa, amma ba sa iya taɓa kome,
ƙafafu, amma ba sa iya tafiya;
ba sa iya ce wani abu da maƙogwaronsu.
8 Masu yinsu za su zama kamar su,
haka kuma zai kasance da duk wanda ya dogara da su.

9 Ya gidan Isra'ila, ku dogara ga UBANGIJI,
shi ne mai taimakonsu da garkuwarsu.
10 Ya gidan Haruna, ku dogara ga UBANGIJI,
shi ne mai taimakonsu da garkuwarsu.
11 Ku da kuke tsoronsa, ku dogara ga UBANGIJI,
shi ne mai taimakonsu da garkuwarsu.

12 UBANGIJI yakan tuna da mu zai kuma albarkace mu.
Zai albarkace gidan Isra'ila,
zai albarkace gidan Haruna,
13 zai albarkace waɗanda suke tsoron UBANGIJI,

manya da ƙanana duka.

14 Bari UBANGIJI yă sa ku ƙaru,
da ku da 'ya'yanku.
15 Bari UBANGIJI yă albarkace ku,
shi Mahalicci sama da ƙasa.

16 Saman sammai na UBANGIJI ne,
amma ya ba da duniya ga mutum.
17 Ba matattu ba ne masu yabon UBANGIJI,
waɗanda suke gangara zuwa wurin da ake shiru;
18 mu ne masu ɗaukaka UBANGIJI,
yanzu da har abada kuma.

Yabi UBANGIJI.*

# Zabura 116

1 Ina ƙaunar UBANGIJI, gama ya ji muryata;
ya ji kukata ta neman jinƙai.
2 Domin ya juye kunnensa gare ni,
zan kira gare shi muddin ina da rai.

3 Igiyoyin mutuwa sun shaƙe ni,
wahalar kabari sun zo a kaina;
na cika da wahala da ɓacin rai.
4 Sai na kira ga sunan UBANGIJI na ce,
"Ya UBANGIJI, ka cece ni!"

5 UBANGIJI mai alheri ne da kuma mai adalci;
Allahnmu yana cike da tausayi.
6 UBANGIJI yana tsare masu tawali'u;
sa'ad da nake cikin tsananin bukata, ya cece ni.

7 Ka kwantar da hankali, ya raina,
gama UBANGIJI mai alheri ne a gare ka.

8 Gama kai, ya UBANGIJI, ka ceci raina daga mutuwa,
idanuna daga hawaye,
ƙafafuna daga tuntuɓe,
9 don in iya tafiya a gaban UBANGIJI
a ƙasar masu rai.

10 Na gaskata, saboda haka na ce,
"An azabtar da ni ƙwarai."
11 Kuma cikin rikicewana na ce,
"Dukan mutane maƙaryata ne."

12 Yaya zan sāka wa UBANGIJI
saboda dukan alherinsa gare ni?

* **Zabura 115:18** Da Ibraniyanci Hallelu Ya

13 Zan daga kwaf na ceto
in kuma kira ga sunan UBANGIJI.
14 Zan cika alkawurana ga UBANGIJI
a gaban dukan mutanensa.

15 Abu mai daraja a gaban UBANGIJI
shi ne mutuwar tsarkakansa.
16 Ya UBANGIJI, da gaske ni bawanka ne;
ni bawanka ne, ɗan baiwarka;
ka ʼyantar da ni daga sarƙoƙi.

17 Zan yi hadayar godiya gare ka
in kuma kira bisa sunan UBANGIJI.
18 Zan cika alkawurana ga UBANGIJI
a gaban dukan mutanensa,
19 a filayen gidan UBANGIJI,
a tsakiyarki, ya Urushalima.

Yabi UBANGIJI.*

# Zabura 117

1 Yabi UBANGIJI, dukanku alʼumma;
ku ɗaukaka shi, dukanku mutane.
2 Gama ƙaunarsa da girma take gare mu,
amincin UBANGIJI kuma madawwami ne har abada.

Yabi UBANGIJI.*

# Zabura 118

1 Ku gode wa UBANGIJI, gama nagari ne shi;
ƙaunarsa madawwamiya ce har abada.

2 Bari Israʼila yǎ ce,
“Kaunarsa madawwamiya ce har abada.”
3 Bari gidan Haruna yǎ ce,
“Kaunarsa madawwamiya ce har abada.”
4 Bari waɗanda suke tsoron UBANGIJI su ce,
“Kaunarsa madawwamiya ce har abada.”

5 Cikin azabata na yi kuka ga UBANGIJI,
ya kuwa amsa ta wurin ʼyantar da ni.
6 UBANGIJI yana tare da ni; ba zan ji tsoro ba.
Me mutum zai yi mini?
7 UBANGIJI yana tare da ni; shi ne mai taimakona.
Zan yi nasara a kan abokan gābana.

8 Ya fi kyau in nemi mafaka a wurin UBANGIJI
da in dogara ga mutum.
9 Ya fi kyau in nemi mafaka a wurin UBANGIJI

* **Zabura 116:19** Da Ibraniyanci Hallelu Ya * **Zabura 117:2** Da Ibraniyanci Hallelu Ya

da in dogara ga sarakuna.
10 Dukan al'ummai sun kewaye ni,
amma a cikin sunan UBANGIJI na hallaka su.
11 Sun kewaye ni a kowane gefe,
amma a cikin sunan UBANGIJI na hallaka su.
12 Sun rufe ni kamar ƙudan zuma,
amma suka mutu nan da nan kamar ƙayayyuwa masu cin wuta;
a cikin sunan UBANGIJI na hallaka su.
13 An ture ni baya na kusa fāɗuwa,
amma UBANGIJI ya taimake ni.
14 UBANGIJI ne ƙarfina da waƙata;
ya zama mai cetona.

15 Sowa ta farin ciki da nasara
sun fito a cikin tentunan adalai,
"Hannun dama na UBANGIJI ya aikata manyan abubuwa!
16 An ɗaga hannun dama na UBANGIJI sama;
hannun dama na UBANGIJI ya aikata manyan abubuwa!"
17 Ba zan mutu ba amma zan rayu,
zan kuwa yi shelar abin da UBANGIJI ya yi.
18 UBANGIJI ya hore ni sosai,
amma bai ba da ni ga mutuwa ba.
19 Buɗe mini ƙofofin adalci;
zan shiga in kuma yi godiya ga UBANGIJI.
20 Wannan ne ƙofar UBANGIJI
inda adalai za su shiga.
21 Zan yi maka godiya, domin ka amsa mini;
ka zama mai cetona.

22 Zabura Dutsen da magina suka ƙi
ya zama mai amfani;
23 UBANGIJI ne ya yi haka,
kuma abu mai daraja ne a idanunmu.
24 Wannan ita ce ranar da UBANGIJI ya yi;
bari mu yi farin ciki mu kuma yi murna a cikinta.

25 Ya UBANGIJI, ka cece mu;
Ya UBANGIJI, ka ba mu nasara.

26 Mai albarka ne shi mai zuwa cikin sunan UBANGIJI.
Daga gidan UBANGIJI muna sa muku albarka.
27 UBANGIJI shi ne Allah
ya kuma sa haskensa ya haskaka a kanmu.
Da kwanoni a hannunmu, muka shiga jerin gwanon biki
ku kai su ƙahoni na bagade.

28 Kai ne Allahna, zan kuwa yi maka godiya;
kai ne Allahna, zan kuwa ɗaukaka ka.

29 Ku gode wa UBANGIJI, gama nagari ne shi;
ƙaunarsa madawwamiya ce har abada.

*

# Zabura 119

*א Alef*

1 Albarka ta tabbata ga waɗanda rayuwarsu ba ta da abin zargi,
waɗanda suke tafiya bisa ga dokar Ubangiji.
2 Albarka ta tabbata ga waɗanda suke kiyaye ƙa'idodinsa
suke kuma nemansa da dukan zuciyarsu.
3 Ba sa yin wani abin da ba daidai ba;
suna tafiya a hanyoyinsa.
4 Ka shimfiɗa farillan
da dole a yi biyayya da su.
5 Kash, da a ce hanyoyina tsayayyu ne
a yin biyayya da ƙa'idodinka mana!
6 Da ba zan sha kunya ba
sa'ad da na lura da dukan umarnanka.
7 Zan yabe ka da zuciya ta gaskiya
yayinda nake koyon dokokinka masu adalci.
8 Zan yi biyayya da ƙa'idodinka;
kada ka yashe ni ɗungum.

*ב Bet*

9 Yaya matashi zai kiyaye hanyarsa da tsabta?
Sai ta yin rayuwa bisa ga maganarka.
10 Na neme ka da dukan zuciyata;
kada ka bar ni in kauce daga umarnanka.
11 Na ɓoye maganarka a cikin zuciyata
don kada in yi maka zunubi.
12 Yabo ya tabbata gare ka, ya Ubangiji;
ka koya mini ƙa'idodinka.
13 Da leɓunana na ba da labarin
dukan dokokin da suka fito bakinka.
14 Na yi farin ciki da bin farillanka
yadda mutum yakan yi farin ciki da arziki mai yawa.
15 Na yi tunani a kan farillanka
na kuma lura da hanyoyinka.
16 Na yi murna a cikin ƙa'idodinka;
ba zan ƙyale maganarka ba.

*ג Gimel*

17 Ka yi alheri ga bawanka, zan kuwa rayu;
zan yi biyayya da maganarka.
18 Ka buɗe idanuna don in iya gani
abubuwan banmamaki a cikin dokarka.
19 Ni baƙo ne a duniya;
kada ka ɓoye mini umarnanka.
20 Zuciyata ta ƙosa saboda marmari
don dokokinka koyaushe.
21 Ka tsawata wa masu fariya, waɗanda suke la'anta
waɗanda kuma suka kauce daga umarnanka.
22 Ka cire mini ba'a da reni,
gama ina kiyaye farillanka.

* **Zabura 119:** Wannan Zabura waƙa ce, ayoyin kowane layi sun fara da irin harufan ɗaya na Ibraniyanci.

23 Ko da yake masu mulki sun zauna tare suna ɓata mini suna,
bawanka zai yi tunani a kan ƙa'idodinka.
24 Farillanka ne abin farin cikina;
su ne mashawartana.

ד *Dalet*

25 An kwantar da ni ƙasa cikin ƙura;
ka kiyaye raina bisa ga maganarka.
26 Na ba da labari hanyoyina ka kuma amsa mini;
ka koya mini ƙa'idodinka.
27 Bari in gane koyarwar farillanka;
sa'an nan zan yi tunani a kan abubuwan banmamakinka.
28 Raina ya gaji da baƙin ciki;
ka ƙarfafa ni bisa ga maganarka.
29 Ka kiyaye ni daga hanyoyin ruɗu;
ka yi mini alheri ta wurin dokokinka.
30 Na zaɓi hanyar gaskiya;
na sa zuciyata a kan dokokinka.
31 Na riƙe farillanka kankan, ya UBANGIJI;
kada ka sa in sha kunya.
32 Ina gudu a kan hanyar umarnanka,
gama ka 'yantar da zuciyata.

ה *He*

33 Ka koya mini Ya UBANGIJI, don in bi ƙa'idodinka;
sa'an nan zan kiyaye su har ƙarshe.
34 Ka ba ni ganewa, zan kuwa kiyaye dokarka
in kuma yi biyayya da ita da dukan zuciyata.
35 Ka bi da ni a hanyar umarnanka,
gama a can zan sami farin ciki.
36 Ka juye zuciyata wajen farillanka
ba wajen riba ta sonkai ba.
37 Ka juye idanuna daga abubuwa marasa amfani;
ka kiyaye raina bisa ga maganarka.
38 Ka cika alkawarinka ga bawanka,
saboda a ji tsoronka.
39 Ka kawar da shan kunyar da nake tsoro,
gama dokokinka nagari ne.
40 Ina marmarin farillanka ƙwarai!
Ka kiyaye raina cikin adalcinka.

ו *Waw*

41 Bari ƙaunarka marar ƙarewa ta zo gare ni, ya UBANGIJI,
cetonka bisa ga alkawarinka;
42 sa'an nan zan amsa wa masu cin mutuncina,
gama na dogara ga maganarka.
43 Kada ka ƙwace maganarka daga bakina,
gama na sa zuciyata a dokokinka.
44 Kullayaumi zan yi biyayya da dokokinka,
har abada abadin.
45 Zan yi ta yawo a sake
gama na nemi farillanka.
46 Zan yi maganar farillanka a gaban sarakuna
ba kuwa za a kunyata ni ba,

47 gama ina farin ciki da umarnanka
saboda ina ƙaunarsu.
48 Na ɗaga hannuwana ga umarnanka, waɗanda nake ƙauna,
ina kuma tunani a kan ƙa'idodinka.

*ז Zayin*

49 Tuna da maganarka ga bawanka,
gama ka ba ni bege.
50 Ta'aziyyata cikin wahalata ita ce
alkawarinka yana kiyaye raina.
51 Masu fariya suna yi mini ba'a ba tare da an hana su ba,
amma ban rabu da dokar ba.
52 Na tuna da dokokinka na tun dā, ya UBANGIJI,
na kuwa sami ta'aziyya a cikinsu.
53 Fushi ya kama ni saboda mugaye,
waɗanda suka keta dokokinka.
54 Ka'idodinka su ne kan waƙata
a duk inda na sauka.
55 Da dare na tuna da sunanka, ya UBANGIJI,
zan kuwa kiyaye dokarka.
56 Wannan shi ne na saba yi,
ina yin biyayya da farillanka.

*ח Het*

57 Kai ne rabona, ya UBANGIJI;
na yi alkawarin in kiyaye maganarka.
58 Na nemi fuskarka da dukan zuciyata;
ka yi mini alheri bisa ga alkawarinka.
59 Na lura da hanyoyina
na kuma mayar da matakaina ga farillanka.
60 Zan gaggauta ba zan ɓata lokaci ba
in yi biyayya da umarnanka.
61 Ko da yake mugaye sun ɗaura ni da igiyoyi,
ba zan manta da dokokinka ba.
62 Da tsakar dare nakan tashi in gode maka
saboda dokokinka masu adalci.
63 Ni aboki ne ga duk mai tsoronka,
ga duk wanda yake bin farillanka.
64 Duniya ta cika da ƙaunarka, ya UBANGIJI;
ka koya mini ƙa'idodinka.

*ט Tet*

65 Ka yi wa bawanka alheri
bisa ga maganarka, ya UBANGIJI.
66 Ka koya mini sani da kuma hukunci mai kyau,
gama na gaskata a umarnanka.
67 Kafin in sha wahala na kauce,
amma yanzu ina biyayya da maganarka.
68 Kai nagari ne, kuma abin da kake yi yana da kyau;
ka koya mini ƙa'idodinka.
69 Ko da yake masu fariya sun shafe ni da ƙarairayi,
na kiyaye farillanka da dukan zuciyata.
70 Zukatansu sun yi tauri da kuma marasa tausayi
amma ina farin ciki a dokarka.
71 Ya yi kyau da na sha wahala

don in koyi ƙa'idodinka.
72 Doka daga bakinka ya fi mini daraja
fiye da azurfa da zinariya guda dubu.

*י Yod*

73 Hannuwanka ne suka yi suka kuma siffanta ni;
ka ba ni ganewa don in koyi umarnanka.
74 Bari waɗanda suke tsoronka su yi farin ciki sa'ad da suke gan ni,
gama na sa zuciyata a maganarka.
75 Ya UBANGIJI na sani, cewa dokokinka masu adalci ne,
kuma cikin aminci ka hore ni.
76 Bari ƙaunarka marar ƙarewa tă yi mini ta'aziyya,
bisa ga alkawarinka ga bawanka.
77 Bari tausayinka yă zo mini don in rayu,
gama dokarka ce farin cikina.
78 Bari masu girman kai su sha kunya saboda abubuwa marasa kyau da suke yi mini ba dalili;
amma zan yi tunani a kan farillanka.
79 Bari waɗanda suke tsoronka su juya gare ni,
waɗanda suka gane da farillanka.
80 Bari zuciyata ta kasance marar abin zargi wajen ƙa'idodinka,
don kada in sha kunya.

*כ Kaf*

81 Raina ya tafke da marmari don cetonka,
amma na sa zuciyata a maganarka.
82 Idanuna sun gaji, suna jiran alkawarinka;
Na ce, "Yaushe za ka ta'azantar da ni?"
83 Ko da yake ni kamar salkar ruwan inabi ne a cikin hayaƙi,
ban manta da ƙa'idodinka ba.
84 Har yaushe bawanka zai yi ta jira?
Yaushe za ka hukunta masu tsananta mini?
85 Masu girman kai sun haƙa mini rami,
sun ƙetare dokarka.
86 Dukan umarnanka abin dogara ne;
ka taimake ni, gama mutane suna tsananta mini ba dalili.
87 Sun kusa gama da ni a duniya,
amma ban bar bin farillanka ba.
88 Ka kiyaye raina bisa ga ƙaunarka,
zan kuwa yi biyayya da farillan bakinka.

*ל Lamed*

89 Maganarka, ya UBANGIJI madawwamiya ce;
tana nan daram a cikin sammai.
90 Amincinka yana cin gaba cikin dukan zamanai;
ka kafa duniya ta kuma dawwama.
91 Dokokinka sun dawwama har yă zuwa yau,
gama dukan abubuwa suna maka hidima.
92 Da ba don dokarka ce farin cikina ba,
da na hallaka a cikin azabana.
93 Ba zan taɓa manta da farillanka ba,
gama ta wurinsu ne ka kiyaye raina.
94 Ka cece ni, gama ni naka ne;
na yi ƙoƙarin neman farillanka.
95 Mugaye suna jira su hallaka ni,

amma zan yi ta tunani a kan farillanka.
96 Ga duk cikakke na ga kāsawa;
amma umarnanka ba su da iyaka.

מ *Mem*

97 Kash, ga yadda nake ƙaunar dokarka!
Ina tunani a kanta dukan yini.
98 Umarnanka suna sa in zama mai hikima fiye da abokan gābana,
gama kullum suna tare da ni.
99 Ina da ganewa sosai fiye da dukan malamaina,
gama ina tunani a kan farillanka.
100 Ina da ganewa fiye da dattawa,
gama ina biyayya da farillanka.
101 Na kiyaye ƙafafuna daga kowace muguwar hanya
domin in yi biyayya da maganarka.
102 Ban rabu da dokokinka ba,
gama kai da kanka ne ka koya mini.
103 Ɗanɗanon maganarka akwai zaki,
sun ma fi zuma zaki a bakina!
104 Na sami ganewa daga farillanka;
saboda haka ina ƙin kowace hanyar da ba daidai ba.

נ *Nun*

105 Maganarka fitila ce ga ƙafafuna
haske kuma a kan hanyata.
106 Na yi rantsuwa na kuma tabbatar da shi,
cewa zan bi dokokinka masu adalci.
107 Na sha wahala sosai;
ka kiyaye raina, ya UBANGIJI, bisa ga maganarka.
108 Ka karɓi yabon bakina da nake yi da yardar rai, ya UBANGIJI,
ka kuwa koya mini dokokinka.
109 Ko da yake kullum ina riƙe da raina a hannuwana,
ba zan manta da dokarka ba.
110 Mugaye sun kafa mini tarko,
amma ban kauce daga farillanka ba.
111 Farillanka su ne gādona har abada;
su ne farin cikin zuciyata.
112 Zuciyata ta shirya a kan kiyaye ƙa'idodinka
har ƙarshe.

ס *Samek*

113 Na ƙi mutane masu baki biyu,
amma ina ƙauna dokarka.
114 Kai ne mafakata da garkuwata;
na sa zuciyata a maganarka.
115 Ku rabu da ni, ku masu aikata mugunta,
don in kiyaye umarnan Allahna!
116 Ka raya ni bisa ga alkawarinka, zan kuwa rayu;
kada ka bari a gwale sa zuciyata.
117 Ka riƙe ni za a kuma cece ni;
kullayaumi zan ɗauka ƙa'idodinka da muhimmanci.
118 Ka ki dukan waɗanda suka kauce daga ƙa'idodinka,
gama yaudararsu banza ne.
119 Dukan mugayen duniya ka zubar kamar datti;
saboda haka nake ƙaunar farillanka.

120 Naman jikina na rawan jiki don tsoronka;
na cika da tsoron dokokinka.

*ע Ayin*

121 Na aikata abin da yake mai adalci da kuma daidai;
kada ka ni a hannun masu danne ni.
122 Ka tabbatar da lafiyar bawanka;
kada ka bar masu girman kai su danne ni.
123 Idanuna sun gaji, da jiran cetonka,
da jiran alkawarinka mai adalci.
124 Ka yi da bawanka bisa ga ƙaunarka
ka kuma koya mini ƙa'idodinka.
125 Ni bawanka ne, ka ba ni fahimi
don in gane farillanka.
126 Lokaci ya yi da za ka yi wani abu, ya UBANGIJI;
ana karya dokarka.
127 Saboda ina ƙaunar umarnanka
fiye da zinariya, kai, fiye da zinariya zalla,
128 saboda kuma ina lura da dukan farillanka da kyau,
na ƙi kowace hanyar da ba daidai ba.

*פ Fe*

129 Farillanka masu banmamaki ne;
saboda haka nake yin biyayya da su.
130 Fassarar maganganunka sukan ba da haske;
sukan ba da ganewa ga marar ilimi.
131 Ina hakkin da bakina a buɗe,
ina marmarin umarnanka.
132 Ka juye wurina ka kuma yi mini jinƙai,
yadda kullum ka yi wa waɗanda suke ƙaunar sunanka.
133 Ka bi da sawuna bisa ga maganarka;
kada ka bar zunubi yǎ mallake ni.
134 Ka fanshe ni daga mutane masu danniya,
don in yi biyayya da farillanka.
135 Ka sa fuskarka ta haskaka a kan bawanka
ka kuma koya mini ƙa'idodinka.
136 Hawaye suna malalowa daga idanuna kamar rafi,
gama ba a biyayya da dokarka.

*צ Tsade*

137 Mai adalci ne kai, ya UBANGIJI,
dokokinka kuma daidai ne.
138 Farillan da ka shimfiɗa masu adalci ne;
su kuma abin dogara ne ƙwarai.
139 Kishina ya cinye ni ɗungum,
gama abokan gābana sun yi biris da maganganunka.
140 An gwada alkawuranka sarai,
bawanka kuwa yana ƙaunarsu.
141 Ko da yake ni ba kome ba ne an kuwa rena ni,
ba na manta da farillanka.
142 Adalcinka dawwammame ne
dokar kuma gaskiya ce.
143 Wahala da damuwa suna a kaina,
amma umarnanka su ne farin cikina.
144 Farillanka daidai ne har abada;

ka ba ni ganewa don in rayu.

*ק Kof*

145 Na yi kira da dukan zuciyata; ka amsa mini, ya UBANGIJI,
zan kuwa yi biyayya da ƙa'idodinka.
146 Na yi kira gare ka; ka cece ni
zan kuwa kiyaye farillanka.
147 Na tashi kafin fitowar rana na kuma yi kukan neman taimako;
na sa zuciyata a maganarka.
148 Ban rufe idanuna ba dukan dare,
don in yi tunani a kan alkawuranka.
149 Ka ji muryata bisa ga ƙaunarka;
ka kiyaye raina, ya UBANGIJI, bisa ga dokokinka.
150 Waɗanda suke ƙirƙiro mugayen dabaru suna nan kusa,
amma suna nesa da dokarka.
151 Duk da haka kana kusa, ya UBANGIJI,
kuma dukan umarnanka gaskiya ne.
152 Tun tuni na koyi daga farillanka
cewa ka kafa su su kasance har abada.

*ר Resh*

153 Ka dubi wahalata ka cece ni,
gama ban manta da dokarka ba.
154 Ka kāre manufata ka kuma fanshe ni,
ka cece rai na kamar yadda ka alkawarta!
155 Ceto yana nesa da mugaye,
gama ba sa neman ƙa'idodinka.
156 Tausayinka da girma yake, ya UBANGIJI;
ka kiyaye raina bisa ga dokokinka.
157 Maƙiya masu yawa ne suke tsananta mini,
amma ban rabu da farillanka ba.
158 Na dubi marasa aminci da ƙyama,
gama ba sa yin biyayya da maganarka.
159 Dubi yadda nake ƙaunar farillanka;
ka kiyaye raina, ya UBANGIJI, bisa ga ƙaunarka.
160 Dukan maganganunka gaskiya ne;
dukan dokokinka masu adalci madawwami ne.

*ש Sin da Shin*

161 Masu mulki suna tsananta mini ba dalili,
amma zuciyata na rawan jiki game da maganarka.
162 Ina farin ciki da alkawarinka
kamar yadda wani kan sami ganima mai girma.
163 Na ƙi ina kuma ƙyamar ƙarya
amma ina ƙaunar dokarka.
164 Sau bakwai a rana ina yabonka
saboda dokokinka masu adalci.
165 Waɗanda suke ƙaunar dokarka suna da babban salama,
kuma babu abin da zai sa su yi tuntuɓe.
166 Ina jiran cetonka, ya UBANGIJI,
ina kuma bin umarnanka.
167 Ina biyayya da farillanka,
gama ina ƙaunarsu ƙwarai.
168 Ina biyayya da farillanka da kuma koyarwarka,
gama dukan hanyoyina sanannu ne gare ka.

ת *Taw*

169 Bari kukata ta zo gare ka, ya UBANGIJI;
ka ba ni ganewa bisa ga maganarka.
170 Bari roƙona yă zo gabanka;
ka cece ni bisa ga alkawarinka.
171 Bari leɓunana su cika da yabonka,
gama ka koya mini ƙa'idodinka.
172 Bari harshena yă rera game da maganarka,
gama dukan umarnanka masu adalci ne.
173 Bari hannunka yă kasance a shirye don yă taimake ni,
gama na zaɓi farillanka.
174 Ina marmarin cetonka, ya UBANGIJI,
dokarka kuwa ita ce farin cikina.
175 Bari in rayu don in yabe ka,
bari kuma dokokinka su raya ni.
176 Na kauce kamar ɓatacciyar tunkiya.
Ka nemi bawanka,
gama ban manta da umarnanka ba.

# Zabura 120

Waƙar haurawa.
1 Na yi kira ga UBANGIJI cikin damuwata,
ya kuwa amsa mini.
2 Ka cece ni, ya UBANGIJI,
daga leɓuna masu ƙarya
da kuma daga harsuna masu yaudara.

3 Me zai yi maka,
me kuma ya fi,
ya kai harshe mai yaudara?
4 Zai hukunta ku da kibiyoyi masu tsini na jarumi,
tare da garwashin wuta na itacen tsintsiya.

5 Kaitona da nake zama a Meshek,
da nake zama a ciki tentunan Kedar!
6 Da daɗewa na zauna
a cikin waɗanda suke ƙin salama.
7 Ni mutum ne mai salama;
amma sa'ad da na yi magana, su sai su yi ta yaƙi.

# Zabura 121

Waƙar haurawa.
1 Na tā da idanuna zuwa wajen tuddai,
ta ina ne taimakona zai zo?
2 Taimakona zai zo daga wurin UBANGIJI,
wanda ya kafa sama da ƙasa.

3 Ba zai bari ƙafarka tă yi santsi ba,
shi da yake tsaronka ba zai yi gyangyaɗi ba;
4 tabbatacce, shi da yake tsaron Isra'ila
ba ya gyangyaɗi ko barci.

5 Ubangiji yana tsaronka,
Ubangiji ne inuwa a hannun damanka;
6 rana ba za tă buge ka cikin yini ba
balle wata da dare.

7 Ubangiji zai kiyaye ka daga dukan masifa,
zai tsare ranka;
8 Ubangiji zai kiyaye shigarka da fitarka
yanzu da har abada kuma.

# Zabura 122

Waƙar haurawa. Ta Dawuda.
1 Na yi farin ciki tare da waɗanda suka ce da ni,
"Bari mu tafi gidan Ubangiji."
2 Kafafunmu suna tsaye
a ƙofofinki, ya Urushalima.

3 An gina Urushalima kamar birnin
da aka yi a harhaɗe wuri guda.
4 A can ne kabilu suke haurawa,
kabilan Ubangiji,
don su yabi sunan Ubangiji
bisa ga farillan da aka ba wa Isra'ila.
5 A can kursiyoyin shari'a yake tsaye,
kursiyoyin gidan Dawuda.

6 Ku yi addu'a don salamar Urushalima,
"Bari waɗanda suke ƙaunarki su zauna lafiya.
7 Bari salama ta kasance a katangarki
zaman lafiya kuma a fadodinki."
8 Saboda 'yan'uwana da kuma abokaina,
zan ce, "Salama tă kasance tare da ke."
9 Saboda gidan Ubangiji Allahnmu,
zan nemi wadatarki.

# Zabura 123

Waƙar haurawa.
1 Na tā da idanuna gare ka,
gare ka da kursiyinka yake cikin sama.
2 Kamar yadda idanun bayi suna duban hannun maigidansu,
kamar yadda idanun baiwa suna duban hannun uwargijiyarta,
haka idanunmu suna duban Ubangiji Allahnmu,
sai ya nuna mana jinƙansa.

3 Ka yi mana jinƙai, ya Ubangiji, ka yi mana jinƙai,
gama mun jimre da reni mai yawa.
4 Mun jimre da wulaƙanci
daga masu girman kai,
reni mai yawa daga masu fariya.

# Zabura 124

Waƙar haurawa. Ta Dawuda.

1 Da ba don UBANGIJI ya kasance a gefenmu ba,
bari Isra'ila yă ce,
2 da ba don UBANGIJI ya kasance a gefenmu ba
sa'ad da aka auka mana,
3 sa'ad da fushinsu ya ƙuna a kanmu,
ai, da sun haɗiye mu da rai;
4 da rigyawa ta kwashe mu,
da ambaliya ta rufe mu.
5 Da ruwa mai hauka
ya share mu ƙaf.

6 Yabo ya tabbata ga UBANGIJI,
wanda bai bari aka yayyage mu da haƙoransu ba.
7 Mun tsira kamar tsuntsu
daga tarkon mai farauta;
an tsinke tarko,
muka kuwa tsira.
8 Taimakonmu yana a sunan UBANGIJI,
Wanda ya yi sama da ƙasa.

# Zabura 125

Waƙar haurawa.
1 Waɗanda suke dogara ga UBANGIJI suna kama da Dutsen Sihiyona,
wanda ba ya jijjiguwa amma dawwammame ne har abada.
2 Kamar duwatsun da sun kewaye Urushalima,
haka UBANGIJI ya kewaye mutanensa
yanzu da har abada kuma.

3 Sandar mulkin mugaye ba zai ci gaba da kasance
a kan ƙasar da take rabon adalai ba,
domin kada masu adalci su yi amfani
da hannuwansu su aikata mugunta.

4 Ka yi alheri, ya UBANGIJI, ga waɗanda suke nagartattu,
ga waɗanda suke masu aikata gaskiya a zuciyarsu.
5 Amma waɗanda suka juye ga karkatattun hanyoyi
UBANGIJI zai kore su tare da masu aikata mugunta.

Salama tă kasance tare da Isra'ila.

# Zabura 126

Waƙar haurawa.
1 Sa'ad da UBANGIJI ya dawo da kamammu zuwa Sihiyona,
mun kasance kamar mutanen da suka yi mafarki.
2 Bakunanmu sun cika da dariya,
harsunanmu da waƙoƙin farin ciki.
Sai ana faɗi a cikin al'ummai,
"UBANGIJI ya aikata manyan abubuwa dominsu."
3 UBANGIJI ya aikata manyan abubuwa dominmu,
mun kuwa cika da farin ciki.

4 Ka maido da wadatarmu, ya UBANGIJI

kamar rafuffuka a Negeb.
5 Waɗanda suka yi shuka da hawaye
za su yi girbi da waƙoƙin farin ciki.
6 Shi da ya fita yana kuka,
riƙe da iri don shuki,
zai dawo da waƙoƙin farin ciki,
ɗauke da dammuna.

# Zabura 127

Waƙar haurawa. Ta Solomon.
1 In ba UBANGIJI ne ya gina gida ba,
masu gininta suna wahala a banza ne.
In ba UBANGIJI ne yake tsaron birni ba,
masu tsaro suna yin tsaro a banza.
2 Banza ne ka farka da wuri
ka koma da latti,
kana fama don abincin da za ka ci,
gama yakan ba da barci ga waɗanda yake ƙauna.

3 ’Ya’ya maza gādo ne daga UBANGIJI,
yara lada ne daga gare shi.
4 Kamar kibiyoyi a hannun jarumi
haka ’ya’ya mazan da aka haifa wa mutum a ƙuruciya.
5 Mai albarka ne mutumin
da korinsa sun cika da su.
Ba za a kunyata su ba
sa’ad da suke ƙarawa da abokan gābansu a ɗakin shari’a.

# Zabura 128

Waƙar haurawa.
1 Masu albarka ne dukan masu tsoron UBANGIJI,
waɗanda suke tafiya a hanyoyinsa.
2 Za ka ci amfanin aikinka;
albarku da wadata za su zama naka.
3 Matarka za tă zama kamar kuringar inabi mai ’ya’ya
a cikin gidanka;
’ya’yanka maza za su zama kamar tohon zaitun
kewaye da teburinka.
4 Ta haka mai albarka yake
wanda yake tsoron UBANGIJI.

5 Bari UBANGIJI ya albarkace ka daga Sihiyona
dukan kwanakin ranka;
bari ka ga wadatar Urushalima,
6 bari kuma ka rayu ka ga ’ya’ya ’ya’yanka.
Salama tă kasance tare da Isra’ila.

# Zabura 129

Waƙar haurawa.
1 Sun yi mini danniya ƙwarai tun ina ƙarami,
bari Isra’ila yă ce,
2 sun yi mini danniya ƙwarai tun ina ƙarami,
amma ba su yi nasara a kaina ba.

3 Manoma sun nome bayana
suka yi kunyoyinsu da tsayi.
4 Amma UBANGIJI mai adalci ne;
ya ’yantar da ni daga igiyoyin mugaye.

5 Bari dukan waɗanda suke ƙin Sihiyona
a juye da su baya da kunya.
6 Bari su zama kamar ciyawa a kan rufi,
wadda takan bushe kafin tă yi girma;
7 da ita mai girbi ba ya iya cika hannuwansa,
balle wanda yake tarawa yă cika hannuwansa.
8 Kada masu wuce su ce,
“Albarkar UBANGIJI ta kasance a kanku;
muna sa muku albarka a cikin sunan UBANGIJI.”

# Zabura 130

Waƙar haurawa.
1 Daga cikin zurfafa na yi kuka gare ka, ya UBANGIJI;
2 Ya Ubangiji, ka ji muryata.
Bari kunnuwanka su saurara
ga kukata ta neman jinƙai.

3 In kai, ya UBANGIJI, za ka lissafta zunubai,
Ya Ubangiji, wa zai tsaya?
4 Amma tare da kai akwai gafartawa,
saboda haka ake tsoronka.

5 Zan jira UBANGIJI, raina zai jira,
kuma a cikin maganarsa na sa zuciyata.
6 Raina na jiran Ubangiji
fiye da yadda mai tsaro yakan jira safiya,
fiye da yadda mai tsaro yakan jira safiya.

7 Ya Isra’ila, sa zuciya ga UBANGIJI,
gama tare da UBANGIJI akwai ƙauna marar ƙarewa
kuma tare da shi akwai cikakkiyar fansa.
8 Shi kansa zai fanshi Isra’ila
daga dukan zunubansu.

# Zabura 131

Waƙar haurawa. Ta Dawuda.
1 Zuciyata ba mai girman kai ba ce, ya UBANGIJI,
idanuna ba sa fariya;
ban dami kaina da manyan al’amura ba
ko abubuwan da suka sha ƙarfina.
2 Amma na haƙura na kuma kwantar da raina;
kamar yaron da aka yaye tare da mahaifiyarsa,
kamar yaron da aka yaye haka raina yake a cikina.

3 Ya Isra’ila, sa zuciyarka ga UBANGIJI
yanzu da har abada kuma.

# Zabura 132

Waƙar haurawa.
1 Ya Ubangiji, ka tuna da Dawuda
da kuma dukan irin wuyan da ya jimre.

2 Ya yi rantsuwa ga Ubangiji
ya kuma yi alkawari ga Maɗaukaki na Yaƙub cewa,
3 “Ba zan shiga gidana
ko in kwanta a gado ba,
4 ba zan ba wa idanuna barci ba,
ba gyangyaɗi wa idanuna,
5 sai na sami wuri wa Ubangiji,
mazauni domin Maɗaukaki na Yaƙub.”

6 Mun ji haka a Efrata,
muka yi ƙaro da shi a filayen Ya’ar,*,†
7 “Bari mu tafi wurin zamansa;
bari mu yi sujada a wurin sa ƙafafunsa,
8 ka tashi, ya Ubangiji, ka kuma zo wurin hutunka,
kai da akwatin alkawarin ƙarfinka.
9 Bari a suturta firistocinka da adalci;
bari tsarkakanka su rera don farin ciki.”

10 Saboda Dawuda bawanka,
kada ka ƙi shafaffenka.

11 Ubangiji ya rantse wa Dawuda
tabbataccen rantsuwa cewa ba zai janye ba cewa,
“Daya daga cikin zuriyarka
zan sa a kan kursiyinka,
12 in ’ya’yanka maza za su kiyaye alkawari
da farillan da na koya musu,
to ’ya’yansu maza za su zauna
a kan kursiyinka har abada abadin.”

13 Gama Ubangiji ya zaɓi Sihiyona,
ya so ta zama mazauninsa,
14 “Wannan shi ne wurin hutuna har abada abadin;
a nan zan zauna ina mulki gama ina son ta,
15 zan albarkace ta da tanade-tanade masu yawa;
matalautanta za su ƙoshi da abinci.
16 Zan suturta firistocinta da ceto,
tsarkakanta kuma kullum za su rera don farin ciki.

17 “A nan zan sa ƙaho‡ ya yi girma wa Dawuda
in kuma kafa fitila saboda shafaffena.
18 Zan suturta abokan gābansa da kunya,
amma rawanin da yake a kansa zai yi ta walƙiya.”

---

* **Zabura 132:6** Wato, Kiriyat Yeyarim † **Zabura 132:6** Ko kuwa mun ji game da shi a Efrata, mun same shi a filayen Ya’ar. (Kuma babu alamar keɓewa kewaye da ayoyi 7-9) ‡ **Zabura 132:17** Kaho a nan yana nufin wani mai ƙarfi, wato, sarki.

# Zabura 133

Waƙar haurawa. Ta Dawuda.
1 Abu mai kyau ne, mai daɗi kuma
sa'ad da 'yan'uwa suna zaman lafiya!

2 Yana kamar mai mai darajar da aka zuba a kai,
yana gangarawa a gemu,
yana gangarawa a gemun Haruna,
har zuwa wuyan rigunansa.
3 Yana kamar raɓar Hermon
da take zubowa a kan Dutsen Sihiyona.
Gama a can UBANGIJI ya tabbatar da albarkarsa,
har ma rai na har abada.

# Zabura 134

Waƙar haurawa.
1 Yabi UBANGIJI, dukanku bayin UBANGIJI
waɗanda kuke hidima da dare a gidan UBANGIJI.
2 Ku tā da hannuwanku a cikin wurinsa mai tsarki
ku kuma yabi UBANGIJI.

3 Bari UBANGIJI, Mahaliccin sama da ƙasa,
ya albarkace ku daga Sihiyona.

# Zabura 135

1 Yabi UBANGIJI.*

Yabi sunan UBANGIJI;
yabe shi, ku bayin UBANGIJI,
2 ku waɗanda kuke hidima a gidan UBANGIJI,
cikin filayen gidan Allahnmu.

3 Yabi UBANGIJI, gama UBANGIJI nagari ne;
rera yabo ga sunansa, gama wannan yana da kyau.
4 Gama UBANGIJI ya zaɓi Yaƙub ya zama nasa,
Isra'ila ya zama mallakarsa mai daraja.

5 Na san cewa UBANGIJI yana da girma,
cewa shugabanmu ya fi dukan alloli girma.
6 UBANGIJI yana yin abin da ya ga dama,
a sammai da kuma a duniya,
cikin tekuna da kuma cikin dukan zurfafansu.
7 Yakan sa gizagizai su taso daga iyakokin duniya;
yakan aika da walƙiya tare da ruwan sama
ya fito da iska daga ɗakunan ajiyarsa.

8 Ya kashe 'ya'yan fari na Masar,
'ya'yan fari na mutane da na dabbobi.
9 Ya aiko da alamu da abubuwan banmamaki a tsirkiyarku, ya Masar,
a kan Fir'auna da kuma dukan bayinsa.

* **Zabura 135:1** Da Ibraniyanci Hallelu Ya; haka ma a ayoyi 3 da 21.

10 Ya bugi al'ummai masu yawa
ya kuma karkashe manyan sarakuna,
11 Sihon sarkin Amoriyawa,
Og sarkin Bashan
da kuma dukan sarakunan Kan'ana,
12 ya kuma ba da ƙasarsa kamar abin gādo,
abin gādo ga mutanensa Isra'ila.

13 Sunanka, ya UBANGIJI, dawwammame ne har abada,
sanin da aka yi maka, ya UBANGIJI, yana nan cikin dukan zamanai.
14 Gama UBANGIJI zai nuna cewa mutanensa ba su da laifi
ya kuma ji tausayin bayinsa.

15 Gumakan al'ummai azurfa ne da zinariya,
da hannuwan mutane suka yi.
16 Suna da bakuna, amma ba sa magana,
idanu, amma ba sa gani;
17 suna da kunnuwa, amma ba sa ji,
ba kuwa numfashi a bakunansu.
18 Waɗanda suka yi su za su zama kamar su,
haka kuma zai zama da dukan waɗanda suke dogara gare su.

19 Ya gidan Isra'ila, yabi UBANGIJI;
Ya gidan Haruna, yabi UBANGIJI;
20 Ya gidan Lawi, yabi UBANGIJI;
ku da kuke tsoronsa, yabi UBANGIJI.
21 Yabo ya tabbata ga UBANGIJI daga Sihiyona,
gare shi wanda yake zama a Urushalima.

Yabi UBANGIJI.

# Zabura 136

1 Ku yi godiya ga UBANGIJI, gama nagari ne shi.
Kaunarsa madawwamiya ce.
2 Ku yi godiya ga Allahn alloli.
Kaunarsa madawwamiya ce.
3 Ku yi godiya ga Ubangijin iyayengiji.
Kaunarsa madawwamiya ce.

4 Gare shi wanda shi kaɗai yake aikata abubuwan banmamaki,
Kaunarsa madawwamiya ce.
5 Wanda ta wurin ganewarsa ya yi sammai,
Kaunarsa madawwamiya ce.
6 Wanda ya shimfiɗa duniya a kan ruwaye,
Kaunarsa madawwamiya ce.
7 Wanda ya yi manyan haskoki,
Kaunarsa madawwamiya ce.
8 Rana don tă yi mulkin yini,
Kaunarsa madawwamiya ce.
9 Wata da taurari kuma don su yi mulkin dare;
Kaunarsa madawwamiya ce.

10 Gare shi wanda ya kashe ’ya’yan fari Masar
Kaunarsa madawwamiya ce.
11 Ya kuma fitar da Isra’ila daga cikinsu
Kaunarsa madawwamiya ce.
12 Da hannu mai ƙarfi da hannu mai iko;
Kaunarsa madawwamiya ce.

13 Gare shi wanda ya raba Jan Teku biyu
Kaunarsa madawwamiya ce.
14 Ya kawo Isra’ila ta tsakiyarsa,
Kaunarsa madawwamiya ce.
15 Amma ya share Fir’auna da mayaƙansa cikin Jan Teku;
Kaunarsa madawwamiya ce.

16 Gare shi wanda ya bi da mutanensa cikin hamada,
Kaunarsa madawwamiya ce.

17 Wanda ya buge manyan sarakuna,
Kaunarsa madawwamiya ce.
18 Ya karkashe manyan sarakuna,
Kaunarsa madawwamiya ce.
19 Sihon sarkin Amoriyawa
Kaunarsa madawwamiya ce.
20 Da kuma Og sarkin Bashan,
Kaunarsa madawwamiya ce.
21 Ya kuma ba da ƙasarsu gādo,
Kaunarsa madawwamiya ce.
22 Gādo ga bawansa Isra’ila;
Kaunarsa madawwamiya ce.

23 Shi wanda ya tuna da mu cikin ƙasƙancinmu
Kaunarsa madawwamiya ce.
24 Ya kuma ’yantar da mu daga abokan gābanmu,
Kaunarsa madawwamiya ce.
25 Wanda kuma ke ba da abinci ga kowace halitta.
Kaunarsa madawwamiya ce.

26 Ku yi godiya ga Allah na sama.
Kaunarsa madawwamiya ce.

# Zabura 137

1 A bakin kogunan Babilon muka zauna muka yi kuka
sa’ad da muka tuna da Sihiyona.
2 A can a kan rassan itatuwa
muka rataye garayunmu,
3 gama a can masu kamunmu suka sa mu yi waƙoƙi,
masu ba mu azaba suka nema waƙoƙin farin ciki;
suka ce, “Ku rera mana ɗaya daga cikin waƙoƙin Sihiyona!”

4 Yaya za mu rera waƙoƙin Ubangiji
a baƙuwar ƙasa?

5 In na manta da ke, ya Urushalima,
bari hannuna na dama manta da iyawarsa.
6 Bari harshena yǎ manne wa rufin bakina
in ban tuna da ke ba,
in ban so Urushalima
farin cikin mafi girma ba.

7 Ka tuna, ya UBANGIJI, abin da mutanen Edom suka yi
a ranar da Urushalima ta fāɗi.
Suka yi ihu suka ce, "A ragargaza ta,
A ragargaza ta har tushenta!"
8 Ya Diyar Babilon, an ƙaddara ke zuwa hallaka,
mai farin ciki ne wanda ya sāka miki
saboda abin da kika yi mana,
9 shi da ya ƙwace jariranki
ya fyaɗa su a kan duwatsu.

# Zabura 138

Ta Dawuda.
1 Zan yabe ka, ya UBANGIJI, da dukan zuciyata;
a gaban "alloli" zan rera yabo.
2 Zan rusuna ta wajen haikalinka mai tsarki
zan kuma yabi sunanka
saboda ƙaunarka da amincinka,
saboda ka ɗaukaka a bisa kome
sunanka da kuma maganarka.
3 Sa'ad da na kira, ka amsa mini;
ka sa na zama mai ƙarfin hali ka kuma ƙarfafa ni.

4 Bari dukan sarakunan duniya su yabe ka, ya UBANGIJI,
sa'ad da suka ji maganganun bakinka.
5 Bari su rera game da hanyoyin UBANGIJI,
gama ɗaukakar UBANGIJI da girma take.

6 Ko da yake UBANGIJI yana bisa, yakan dubi kāsassu,
amma tun da nesa ya san masu girman kai.
7 Ko da na yi tafiya a tsakiyar wahala,
kana kiyaye raina;
ka miƙa hannunka a kan fushin maƙiyana,
da hannunka na dama ka cece ni.
8 UBANGIJI zai cika manufarsa a kaina;
ƙaunarka, ya UBANGIJI, madawwamiya ce har abada,
kada ka ƙyale ayyukan hannuwanka.

# Zabura 139

Don mai bi da kaɗe-kaɗe. Ta Dawuda. Zabura ce.
1 Ya UBANGIJI, ka bincike ni
ka kuwa san ni.
2 Ka san sa'ad da na zauna da sa'ad da na tashi;
ka san tunanina daga nesa.
3 Ka san fitata da kuma kwanciyata;
ka saba da dukan hanyoyina.

4 Kafin in yi magana da harshena
ka santa gaba ɗaya, ya UBANGIJI.
5 Ka kewaye ni, gaba da baya;
ka sa hannunka a kaina.
6 Irin wannan sanin game da ni ya fi ƙarfin magana,
ya fi ƙarfi in gane.

7 Ina zan tafi daga Ruhunka?
Ina zan gudu in tafi daga gabanka?
8 In na haura zuwa sammai, kana a can;
in na yi gado a zurfafa, kana a can.
9 In na tashi a fikafikan safiya,
in na sauka a gefe mai nisa na teku,
10 can ma hannunka zai bishe ni,
hannunka na dama zai riƙe ni gam.
11 In na ce, "Tabbatacce duhu zai ɓoye ni
haske kuma zai zama dare kewaye da ni,"
12 duhu ma ba zai zama duhu gare ka ba;
dare zai haskaka kamar rana,
gama duhu ya yi kamar haske gare ka.

13 Gama ka halicci ciki-cikina;
ka gina ni gaba ɗaya a cikin mahaifar mahaifiyata.
14 Ina yabonka domin yadda ka yi ni abin tsoro ne da kuma abin mamaki;
ayyukanka suna da banmamaki,
na san da haka sosai.
15 Kasusuwana ba a ɓoye suke a gare ka ba
sa'ad da aka yi ni asirce.
Sa'ad da saƙa ni gaba ɗaya a zurfafan duniya.
16 Idanunka sun ga jikina marar fasali;
dukan kwanakin da aka tsara mini a rubuce suke a littafinka
kafin ɗayansu yă kasance.
17 Tunaninka suna da daraja gare ni, ya Allah!
Yawansu ba su da iyaka!
18 A ce zan iya ƙirgansu,
za su fi yashin teku yawa.
Sa'ad da na farka, ina nan tare da kai har yanzu.

19 Da kawai za ka kashe mugaye, ya Allah!
Ku rabu da ni, ku masu kisankai!
20 Suna magana game da kai da mugun nufi;
maƙiyanka suna ɗaukan sunanka a banza.
21 Ba ina ƙin masu ƙinka ba, ya UBANGIJI,
ina kuma ƙyamar waɗanda suke tayar maka ba?
22 Ba ni da wani abu da nake musu sai kiyaye kawai;
na ɗauke su abokan gābana.
23 Ka bincike ni, ya Allah ka kuma san zuciyata;
ka gwada ni ka kuma san damuwata.
24 Duba ko akwai wani laifi a cikina,
ka bishe ni a madawwamiyar hanya.

# Zabura 140

Don mai bi da kaɗe-kaɗe. Zabura ta Dawuda.
1 Ka cece ni, ya UBANGIJI, daga mugaye;
ka tsare ni daga mutane masu rikici,
2 masu shirya maƙarƙashiya a zukatansu
suna kuma kawo yaƙi kullum.
3 Suna sa harsunansu su yi kaifi kamar na maciji;
dafin gamsheƙa yana a leɓunansu.
Sela

4 Ka kiyaye ni, ya UBANGIJI, daga hannuwan mugaye;
ka tsare ni daga mutane masu rikici
waɗanda suke shirin kwashe ni a ƙafafu.
5 Masu girman kai sun sa mini tarko;
sun shimfiɗa igiyoyin ragarsu
sun kuma shirya mini tarko a hanyata.
Sela

6 Ya UBANGIJI, na ce maka, "Kai ne Allahna."
Ka ji kukata ta neman jinƙai, ya UBANGIJI.
7 Ya UBANGIJI Mai Iko Duka, mai fansana mai ƙarfi,
wanda yake garkuwoyin kaina a ranar yaƙi.
8 Kada ka biya wa mugaye bukatunsu, ya UBANGIJI;
kada ka bar shirinsu su yi nasara,
in ba haka ba za su yi fariya.
Sela

9 Bari kawunan waɗanda suka kewaye ni
su rufu da masifun da leɓunansu suka jawo.
10 Bari garwashin wuta yă zubo a kansu;
bari a jefar da su cikin wuta,
cikin rami mai zurfi, kada su sāke tashi.
11 Kada masu ɓata suna su taɓa kahu a ƙasar;
bari masifa ta farauci mutane masu rikici.

12 Na san cewa UBANGIJI ya shirya wa matalauta adalci
yana kuma yi wa mabukata adalci.
13 Tabbatacce masu adalci za su yabi sunanka
masu aikata gaskiya kuma za su zauna a gabanka.

# Zabura 141

Zabura ta Dawuda.
1 Na yi kira gare ka, ya UBANGIJI; ka zo da sauri.
Ka ji muryata sa'ad da na yi kira.
2 Bari a sa addu'ata a gabanka kamar turaren ƙonawa;
bari ɗagawa hannuwana ta zama kamar hadayar yamma.

3 Ka sa mai tsaro a bakina, ya UBANGIJI;
ka yi tsaron ƙofar leɓunana.
4 Kada ka bar zuciyata ta juya ga yin abin da yake mugu,
ta sa kai ga aikata mugayen ayyuka
tare da mutane masu aikata mugunta;

kada ka bari in ci abincinsu.

5 Bari mutum mai adalci yă buge ni, alheri ne;
bar shi yă tsawata mini, mai ne a kaina.
Kaina ba zai ƙi shi ba,
duk da haka addu'ata kullum tana gāba da mugayen ayyuka.

6 Za a jefar da masu mulkinsu ƙasa daga ƙwanƙolin dutse,
mugaye kuwa za su san cewa maganata daidai ne.
7 Za su ce, "Kamar yadda mutum kan yi huda yă tsage ƙasa,
haka aka watsar da ƙasusuwanmu a bakin kabari."

8 Amma na kafa idanuna a kanka, ya UBANGIJI Mai Iko Duka;
a cikinka ina neman mafaka, kada ka miƙa ni ga mutuwa.
9 Ka kiyaye ni daga tarkon da aka sa mini,
daga tarkon da mugaye suka sa.
10 Bari mugaye su fāɗa a cikin ragarsu,
amma bari ni in zo in wuce lafiya.

# Zabura 142

*Maskil* ne* ta Dawuda. Sa'ad da yake cikin kogo. Addu'a ce.
1 Na yi kuka mai ƙarfi ga UBANGIJI;
na tā da muryata ga UBANGIJI neman jinƙai.
2 Na kawo gunagunina a gabansa;
a gabansa na faɗa wahalata.

3 Sa'ad da ƙarfina ya kāre a cikina,
kai ne wanda ya san hanyata.
A hanyar da nake tafiya
mutane sun kafa mini tarko.
4 Duba ta damata ka gani;
babu wanda ya kula da ni.
Ba ni da mafaka;
babu wanda ya kula da raina.

5 Na yi kuka gare ka, ya UBANGIJI;
Na ce, "Kai ne mafakata,
rabona a ƙasar masu rai."

6 Ka saurari kukata,
gama ina cikin matsananciyar bukata;
ka cece ni daga waɗanda suke fafarata,
gama sun fi ni ƙarfi sosai.
7 Ka 'yantar da ni daga kurkuku,
don in yabi sunanka.
Ta haka masu adalci za su taru kewaye da ni
saboda alherinka gare ni.

# Zabura 143

Zabura ta Dawuda.

* **Zabura 142:** Kan maganar, mai yiwuwa kalmar waƙa ce.

1 Ya UBANGIJI, ka ji addu'ata,
ka saurari kukata don neman jinƙai;
cikin amincinka da adalcinka
ka amsa mini.
2 Kada ka gabatar da bawanka a gaban shari'a,
gama babu wani mai rai da yake adali a gabanka.
3 Abokin gāba yana fafarata,
ya murƙushe ni har ƙasa;
ya sa ina zama a cikin duhu
kamar waɗanda suka mutu tun tuni.
4 Ta haka ƙarfina ya ƙare a cikina
zuciyata ta damu ƙwarai.
5 Na tuna da kwanakin baya
na yi tunani a kan dukan ayyukanka
na kuma lura da abin da hannuwanka suka yi.
6 Na buɗe hannuwana gare ka;
raina yana jin ƙishinka kamar busasshiyar ƙasa.
Sela

7 Ka amsa mini da sauri, ya UBANGIJI;
ƙarfina ya ƙare.
Kada ka ɓoye fuskarka daga gare ni
in ba haka ba zan zama kamar waɗanda suka gangara zuwa rami.
8 Bari safiya ta kawo mini maganar ƙaunarka marar ƙarewa,
gama na sa zuciyata a gare ka.
Ka nuna mini hanyar da zan bi,
gama a gare ka na miƙa raina.
9 Ka cece ni daga abokan gābana, ya UBANGIJI,
gama na ɓoye kaina a gare ka.
10 Ka koya mini in yi nufinka,
gama kai ne Allahna;
bari nagarin Ruhunka
yǎ bi da ni a ƙasar da ba gargaɗa.

11 Saboda sunanka, ya UBANGIJI, ka kiyaye raina;
a cikin adalcinka, ka fid da ni daga wahala.
12 A cikin ƙaunarka marar ƙarewa, ka rufe bakunan abokan gābana;
ka hallaka dukan maƙiyana,
gama ni bawanka ne.

# Zabura 144

Ta Dawuda.
1 Yabo ya tabbata ga UBANGIJI dutsena,
wanda ya horar da hannuwana don yaƙi,
yatsotsina don faɗa.
2 Shi ne Allah mai ƙaunata da kuma kagarata,
katangata da mai cetona,
garkuwata, wanda nake neman mafaka daga gare shi,
wanda ya sa mutane a ƙarƙashina.

3 Ya UBANGIJI, wane ne mutum da ka kula da shi,

ɗan mutum da har za ka yi tunaninsa?
4 Mutum yana kama da numfashi;
kwanakinsa suna wucewa kamar inuwa.

5 Ka tsage sammanka, ya UBANGIJI, ka sauko;
ka taɓa duwatsu, domin su yi hayaƙi.
6 Ka aiko da walƙiya ka watsar da abokan gāba;
ka karɓa kibiyoyinka ka sa su gudu.
7 Ka miƙa hannunka daga bisa;
ka cece ni ka kuma kuɓutar da ni
daga manyan ruwaye,
daga hannuwan baƙi
8 waɗanda bakunansu sun cika da ƙarya,
waɗanda hannuwansu na dama masu ruɗu ne.

9 Zan rera sabuwar waƙa gare ka, ya Allah;
a kan molo mai tsirkiya goma zan yi maka kiɗi,
10 ga Wannan wanda yake ba wa sarakuna nasara,
wanda ya cece bawansa Dawuda.

Daga takobin kisa. 11 Ka cece ni ka kuma kuɓutar da ni
daga hannuwan baƙi
waɗanda bakunansu sun cika da ƙarya,
waɗanda hannuwansu na dama masu ruɗu ne.

12 Ta haka ʼyaʼyanmu maza a ƙuruciyarsu
za su zama kamar tsire-tsiren da aka kula da su,
ʼyaʼyanmu mata kuma za su zama kamar ginshiƙai
da sassaƙa don adon fada.
13 Rumbunanmu za su cika
da kowane irin tanadi.
Tumakinmu za su ƙaru ninki dubu,
ninki dubu goma-goma a filayenmu;
14 shanunmu za su ja kaya masu nauyi.*
Ba za a sami tashin hankali a katangarmu ba,
ba zuwan zaman bauta,
ba jin kukan damuwa a titunanmu.
15 Masu albarka ne mutanen da wannan zai zama haka;
masu albarka ne mutanen da Allah ne UBANGIJI.
*

# Zabura 145

Zabura ce ta yabo. Ta Dawuda.
1 Zan ɗaukaka ka, ya Allahna, Sarki;
zan yabi sunanka har abada abadin.
2 Kowace rana zan yabe ka
in kuma ɗaukaka sunanka har abada abadin.

3 UBANGIJI da girma yake ya kuma cancanci yabo
girmansa ya fi ƙarfin ganewar mutum.

* **Zabura 144:14** Ko kuwa manyanmu za su kahu daram * **Zabura 145:** Wannan Zabura waƙa ce, ayoyin waɗanda suka (haɗa da aya 13b) sun fara da irin harufa ɗaya bayan ɗaya na Ibraniyanci.

4 Tsara guda za tă yi maganar ayyukanka ga wata tsara;
za su yi magana game da manyan ayyukanka.
5 Za su yi zancen ɗaukakarka mai daraja,
zan kuma yi tunani a kan ayyukanka masu banmamaki.
6 Za su yi magana game da ikon ayyukanka masu bantsoro,
zan kuma yi shelar manyan ayyukanka.
7 Za su yi bikin yalwar alherinka
suka kuma rera adalcinka da farin ciki.

8 UBANGIJI mai alheri da kuma tausayi,
mai jinkirin fushi cike kuma da ƙauna.

9 UBANGIJI nagari ne ga duka;
yana tausayin dukan abubuwan da ya yi.
10 Dukan abubuwan da ka yi za su yabe ka, ya UBANGIJI;
tsarkakanka za su ɗaukaka ka.
11 Za su yi maganar ɗaukakar mulkinka
za su kuma yi zancen ikonka,
12 saboda dukan mutane su san manyan ayyukanka
da ɗaukakar darajar mulkinka.
13 Mulkinka madawwamin mulki ne,
sarautarka kuma za tă dawwama cikin dukan zamanai.

UBANGIJI mai aminci ne ga dukan alkawuransa
mai ƙauna kuma ga dukan abubuwan da ya yi.
14 UBANGIJI yana riƙe da dukan waɗanda suka faɗi
yana kuma ɗaga dukan waɗanda aka rusunar da su ƙasa.
15 Idanun kowa yana dogara gare ka,
kana kuma ba su abincinsu a lokacin da ya dace.
16 Ka buɗe hannunka
ka kuma ƙosar da sha'awar kowane abu mai rai.

17 UBANGIJI mai adalci ne cikin dukan hanyoyinsa
yana kuma nuna ƙauna ga dukan abubuwan da ya yi.
18 UBANGIJI yana kusa da kowa da ya kira gare shi,
ga duk wanda ya kira gare shi cikin gaskiya.
19 Yakan cika sha'awar waɗanda suke tsoronsa;
yakan ji kukansu yă kuma cece su.
20 UBANGIJI yakan lura da dukan waɗanda suke ƙaunarsa,
amma dukan mugaye zai hallaka su.

21 Bakina zai yi magana cikin yabon UBANGIJI.
Bari kowace halitta ta yabi sunansa mai tsarki
har abada abadin.

# Zabura 146

1 Yabi UBANGIJI.*

Yabi UBANGIJI, ya raina.

---

* **Zabura 146:1** Da Ibraniyanci Hallelu Ya; haka ma a aya 10.

2 Zan yabi UBANGIJI dukan kwanakina;
zan rera yabo ga Allahna muddin raina.
3 Kada ka sa zuciyarka ga sarakuna,
ga mutane masu mutuwa, waɗanda ba sa iya ceto.
4 Sa'ad da numfashinsu ya rabu da su sai su koma ƙasa;
a wannan rana shirye-shiryensu sun zama banza.
5 Mai albarka ne wanda Allah na Yaƙub ne taimakonsa,
wanda sa zuciyarsa yana a kan UBANGIJI Allahnsa.

6 Mahaliccin sama da ƙasa,
teku, da kome da yake cikinsu,
UBANGIJI, wanda yake mai aminci har abada.
7 Yakan biya bukatun mutanen da aka danne
ya kuma ba da abinci ga mayunwata.
UBANGIJI yakan 'yantar da 'yan kurkuku,
8 UBANGIJI yakan ba wa makafi ido,
UBANGIJI yakan ɗaga waɗanda aka rusunar da su ƙasa,
UBANGIJI yana ƙaunar masu adalci.
9 UBANGIJI yana tsaron baƙi
yana kuma lura da marayu da kuma gwauruwa,
amma yakan lalatar da hanyoyin mugaye.

10 UBANGIJI yana mulki har abada,
Allahnki, ya Sihiyona, daga zamani zuwa zamani.

Yabi UBANGIJI.

# Zabura 147

1 Yabi UBANGIJI.*

Yana da kyau a rera yabai ga Allahnmu,
abu mai daɗi ne daidai ne kuma a yabe shi!

2 UBANGIJI ya gina Urushalima;
ya tattara kamammu na Isra'ilan da aka kai bauta.
3 Ya warkar da masu raunanar zuciya
ya ɗaɗɗaura miyakunsu.
4 Ya lissafta yawan taurari
ya kuma kira kowannensu da suna.
5 Shugabanmu mai girma ne mai iko duka;
ganewarsa ba shi da iyaka.
6 UBANGIJI yana kula da masu sauƙinkai
yakan yar da mugaye a ƙasa.

7 Rera wa UBANGIJI waƙar godiya;
ku kada garaya ga Allahnmu.

8 Ya rufe sararin sama da gizagizai;
yana tanada wa duniya ruwan sama

* **Zabura 147:1** Da Ibraniyanci Hallelu Ya; haka ma a aya 20.

yana kuma sa ciyawa tă yi girma a kan tuddai.
9 Yakan tanada wa shanu abinci
da kuma saboda ʼyaʼyan hankaki saʼad da suka yi kira.

10 Jin daɗinsa ba ya a ƙarfin doki,
balle farin cikinsa yă kasance a ƙafafun mutum;
11 UBANGIJI yakan yi farin ciki a waɗanda suke tsoronsa,
waɗanda suke sa zuciya a ƙaunarsa marar ƙarewa.

12 Ki ɗaukaka UBANGIJI, ya Urushalima;
ki yabi Allahnki, ya Sihiyona.

13 Gama yana ƙarfafa ƙyamaren ƙofofinki
yana kuma albarkace mutanenki a cikinki.
14 Yana ba da salama ga iyakokinki
yana kuma ƙosar da ke da alkama mafi kyau.

15 Yana ba da umarninsa ga duniya;
maganarsa tana tafiya da sauri.
16 Yana shimfiɗa ƙanƙara kamar ulu
yă kuma watsar da hazo kamar toka.
17 Yana zuba ƙanƙara kamar ƙananan duwatsu.
Wa zai iya jure wa sanyin da ya aiko?
18 Yakan aiki maganarsa ta kuwa narkar da su;
yakan tā da iskarsa, ruwaye kuwa su gudu.

19 Ya bayyana maganarsa ga Yaƙub,
dokokinsa da ƙaʼidodinsa ga Israʼila.
20 Bai yi wannan ga wata alʼumma ba;
ba su san dokokinsa ba.

Yabi UBANGIJI.

# Zabura 148

1 Yabi UBANGIJI.*

Yabi UBANGIJI daga sammai,
yabe shi a bisa sammai.
2 Yabe shi, dukanku malaʼikunsa,
yabe shi, dukanku rundunarsa na sama.
3 Yabe shi, rana da wata,
yabe shi, dukanku taurari masu haskakawa.
4 Yabe shi, ku bisa sammai
da kuma ku ruwan bisa sarari.

5 Bari su yabi sunan UBANGIJI,
gama ya umarta aka kuwa halicce su.
6 Ya sa su a wurarensu har abada abadin;
ya ba da umarnin da ba zai taɓa shuɗe ba.

* **Zabura 148:1** Da Ibraniyanci Hallelu Ya; haka ma a aya 14.

7 Yabi UBANGIJI daga duniya,
ku manyan halittun teku da kuma dukan zurfafan teku,
8 walƙiya da ƙanƙara, dusar ƙanƙara da gizagizai,
hadirin iskar da suke biyayya da umarnansa,
9 ku duwatsu da dukan tuddai,
itatuwa masu ʼyaʼya da dukan alʼul,
10 namun jeji da dukan dabbobin gida,
ƙanana halittu da tsuntsaye masu firiya,
11 sarakunan duniya da dukan alʼummai,
ku sarakuna da dukan masu mulkin duniya,
12 samari da ʼyan mata,
tsofaffi da yara.

13 Bari su yabi sunan UBANGIJI,
gama sunansa ne kaɗai mafi ɗaukaka;
darajarsa ta fi ƙarfin duniya da sammai.
14 Ya tayar wa mutanensa ƙaho,†
yabon dukan tsarkakansa,
na Israʼila, mutanen da suke kurkusa da zuciyarsa.

Yabi UBANGIJI.

# Zabura 149

1 Yabi UBANGIJI.*

Ku rera sabuwar waƙa ga UBANGIJI,
yabonsa a cikin taron tsarkaka.

2 Bari Israʼila su yi farin ciki da Mahaliccinsu;
bari mutanen Sihiyona su yi murna da Sarkinsu.
3 Bari su yabi sunansa tare da rawa
suna kuma yin kiɗi gare shi da ganga da garaya.
4 Gama UBANGIJI yana jin daɗin mutanensa;
yakan darjanta masu sauƙinkai da ceto.
5 Bari tsarkaka su yi farin ciki a wannan bangirma
su kuma rera don farin ciki a kan gadajensu.

6 Bari yabon Allah yă kasance a bakunansu
takobi mai kaifi kuma a hannuwansu,
7 don su ɗau fansa a kan alʼummai
da kuma hukunci a kan mutane,
8 don su ɗaura sarakuna da sarƙoƙi,
manyan garinsu da sarƙoƙin ƙarfe,
9 don su yi hukuncin da aka rubuta a kansu.
Wannan ne ɗaukakar dukan tsarkakansa.

Yabi UBANGIJI.

† **Zabura 148:14** Kaho a nan na nuna wani mai ƙarfi, wato, sarki.
* **Zabura 149:1** Da Ibraniyanci Hallelu Ya; haka ma a aya 9.

# Zabura 150

1 Yabi UBANGIJI.*

Yabi Allah a cikin wurinsa mai tsarki;
yabe shi a cikin sammai na ikonsa.
2 Yabe shi saboda ayyukansa masu iko;
yabe shi saboda mafificin girmansa.
3 Yabe shi da ƙarar kakaki,
yabe shi da garaya da molo,
4 yabe shi da ganga kuna taka rawa,
yabe shi da kayan kiɗi na tsirkiya kuna kuma busa,
5 yabe shi da kuge mai ƙara,
yabe shi da kuge masu ƙara sosai.

6 Bari kowane abu mai numfashi yǎ yabi UBANGIJI.

Yabi UBANGIJI.

* **Zabura 150:1** Da Ibraniyanci Hallelu Ya; haka ma a aya 6.

# Karin Magana
## Gabatarwa, manufa da kuma kan magana

1 Karin maganar Solomon ɗan Dawuda, sarkin Isra'ila.
2 Ga karin magana da za su taimake ka don samun hikima da horo;
don ganewa kalmomi masu zurfi;
3 don neman rayuwa ta horo da kuma ta hankali,
kana yin abin da yake daidai, mai adalci da kuma wanda ya dace;
4 don sa marar azanci yǎ yi hankali,
yǎ sa matasa su sani, su kuma iya rarrabewa,
5 bari masu hikima su saurara, su kuma ƙara ga saninsu,
bari masu tunani kuma su sami jagora,
6 don su fahimci karin magana da kuma misalai,
kalmomi da kuma kacici-kacici masu hikima.

7 Tsoron Ubangiji shi ne masomin ilimi,
amma wawaye* sun rena hikima da horo.

## Gargaɗi don a rungumi hikima

*Jan kunne game da jaraba*

8 Ɗana, ka saurari umarnin mahaifinka
kada kuma ka ƙyale koyarwar mahaifiyarka.
9 Za su zama kayan ado don su inganta ka
da kuma sarƙar wuya don su yi wa wuyanka ado.

10 Ɗana, in masu zunubi sun jarabce ka,
kada ka yarda.
11 In suka ce, "Zo mu tafi;
mu yi kwanton ɓauna, mu nemi wani mu kashe,
mu fāɗa wa marasa laifi;
12 mu haɗiye su da rai gaba ɗaya kamar kabari,
kamar waɗanda suke gangarawa zuwa rami;
13 za mu sami dukiya masu daraja iri-iri,
mu kuma cika gidajenmu da ganima;
14 ka haɗa kai da mu,
za mu kuwa raba abin da muka sato"
15 ɗana, kada ka tafi tare da su,
kada ka taka ƙafarka a hanyarsu;
16 gama ƙafafunsu kan yi sauri ga yin zunubi,
suna saurin yin kisankai.
17 Ba shi da amfani a kafa tarko
a idanun dukan tsuntsaye!
18 Waɗannan irin mutane kansu suke kafa wa tarko;
ba sa kama kome, sai rayukansu!
19 Dukan waɗanda suke neman ribar da ba a samu a hanya mai kyau;
ƙarshen wannan yakan ɗauke rayukansu.

---

* **1:7** Kalmomin Ibraniyancin da aka rubuta wawa a cikin Littafi Karin Magana, da kuma ko'ina a cikin Tsohon Alkawari sau da yawa, yana nufin wani wanda ya rasa cikakken ɗa'a ne.

*Jan kunne game da ƙin hikima*
20 Hikima tana kira da ƙarfi a kan titi,
tana ɗaga muryarta a dandalin taron jama'a;
21 tana kira da ƙarfi a kan brtituna masu surutu,†
tana yin jawabinta a hanyoyin shiga gari.

22 "Har yaushe ku da kuke marasa azanci‡ za ku ci gaba a hanyoyinku marasa azanci?
Har yaushe ku masu ba'a za ku yi ta murna cikin ba'arku
wawaye kuma ku ƙi ilimi?
23 Da a ce kun saurari tsawatata,
da na faɗa muku dukan abin da yake zuciyata
in kuma sanar da ku tunanina.
24 Amma da yake kun ƙi ni sa'ad da na yi kira
ba kuma wanda ya saurara sa'ad da na miƙa hannuna,
25 da yake kun ƙi dukan shawarata
ba ku kuma yarda da tsawatata ba,
26 Zan yi muku dariya sa'ad da masifa ta same ku,
zan yi muku ba'a sa'ad da bala'i ya same ku,
27 sa'ad da bala'i ya sha kanku kamar hadiri,
sa'ad da masifa ta share ku kamar guguwa,
sa'ad damuwa da wahala suka mamaye ku.

28 "Sa'an nan za su kira gare ni amma ba zan amsa ba;
za su neme ni amma ba za su same ni ba.
29 Da yake sun ƙi sani
ba su kuwa zaɓi tsoron UBANGIJI ba,
30 da yake ba su karɓi shawarata ba
suka kuwa yi kunnen ƙashi ga tsawatata,
31 za su sami sakayyar abubuwan da suka yi
su kuma ƙoshi da sakayyar makircinsu.
32 Gama rashin hankalin marasa azanci zai kashe su,
rashin kulawar wawaye kuma zai hallaka su;
33 amma duk wanda ya saurare ni, zai zauna lafiya
yǎ kuma kasance da rai kwance, ba tare da tsoron lahani ba."

# 2

*Ribar ɗa'ar hikima*
1 Ɗana, in ka yarda da kalmomina
ka kuma ajiye umarnaina a cikinka,
2 kana kasa kunne ga abin da yake na hikima,
kana kuma yin ƙoƙari ka fahimce shi,
3 in kuma ka kira ga tsinkaya
ka kuma kira da ƙarfi don ganewa,
4 in ka neme shi yadda ake neman azurfa
ka kuma neme shi kamar yadda ake neman ɓoyayyiyar dukiya,
5 to, za ka gane tsoron UBANGIJI
ka kuma sami sanin Allah.
6 Gama UBANGIJI yana ba da hikima,

† **1:21** Da Ibraniyanci; Seftuwajin / a bisa katanga ‡ **1:22** Kalmar Ibraniyancin da aka rubuta marar azanci a cikin Littafin Kari Magana gaba ɗaya tana nufin marar ɗa'a da kuma wanda yana aikata mugunta ne.

daga bakinsa kuma, sani da ganewa sukan fito.
7 Yana riƙe da nasara a ma'aji don masu yin gaskiya,
shi ne mafaka ga waɗanda tafiyarsu ba ta da laifi,
8 gama yana tsare abin da masu adalci suke bukata
yana kuma tsare hanyar amintattunsa.

9 Sa'an nan za ku fahimci abin da yake daidai da abin da yake na adalci
da abin da yake gaskiya, da kowace hanya mai kyau.
10 Gama hikima za tă shiga cikin zuciyarka,
sani kuma zai faranta maka rai.
11 Tsinkaya za tă tsare ka,
ganewa kuma za tă yi maka jagora.

12 Hikima za tă cece ka daga hanyoyin mugayen mutane,
daga kalmomin mutane masu ɓatanci,
13 waɗanda suke barin miƙaƙƙun hanyoyi
don su yi tafiya a hanyoyi masu duhu,
14 waɗanda suke jin daɗin yin abin da ba shi da kyau
suna kuma farin ciki a mugayen ɓatanci,
15 waɗanda hanyoyinsu karkatattu ne
waɗanda kuma suke cuku-cuku a hanyoyinsu.

16 Zai kiyaye ku kuma daga mazinaciya,
daga mace mai lalata, mai ƙoƙarin kama ka da daɗin bakinta,
17 wadda ta bar mijin ƙuruciyarta
ta kuma ƙyale alkawarin da ta yi a gaban Allah.*
18 Gama gidanta yana kai ga mutuwa
hanyarta kuma ga ruhohin matattu.
19 Duk wanda ya ziyarce ta ba ya ƙara komowa
ba zai ƙara komowa ga hanyar rai.

20 Don haka dole ku yi tafiya a hanyoyin mutanen kirki
ku kuma yi ta bi hanyoyin adalai.
21 Gama masu aikata gaskiya za su zauna a cikin ƙasar,
marasa laifi kuma za su kasance a cikinta;
22 amma za a fid da mugaye daga ƙasar,
za a tumɓuke marasa aminci kuma daga gare ta.

# 3

*Karin ribar hikima*

1 Ɗana, kada ka manta da koyarwata,
amma ka kiyaye umarnaina a cikin zuciyarka,
2 gama za su ƙara maka tsawon rai da shekaru masu yawa
su kuma kawo maka wadata.

3 Kada ka bar ƙauna da aminci su rabu da kai;
ka ɗaura su kewaye da wuyanka,
ka rubuta su a allon zuciyarka.
4 Sa'an nan za ka sami tagomashi da kuma suna mai kyau

* **2:17** Ko kuwa alkawarin Allahnta

a gaban Allah da kuma a gaban mutane.

5 Ka dogara ga UBANGIJI da dukan zuciyarka
kada kuma ka dangana ga ganewarka;
6 cikin dukan hanyoyinka ka amince da shi,
zai kuwa sa hanyoyinka su miƙe.*

7 Kada ka zama mai hikima a ganinka;
ka ji tsoron UBANGIJI ka kuma guji mugunta.
8 Wannan zai ba wa jikinka lafiya
yă kuma adana ƙasusuwanka.

9 Ka girmama UBANGIJI da dukan dukiyarka,
ta wurin miƙa masa nunan fari na dukan amfanin gonarka;
10 ta haka rumbunanka za su cika har su zuba,
randunanka kuma su cika har baki da sabon ruwan inabi.

11 Ɗana, kada ka rena horon UBANGIJI
kada kuma ka ƙi tsawatawarsa,
12 domin UBANGIJI yakan hori waɗanda yake ƙauna,
kamar yadda mahaifi yake yin wa ɗa da yake fariya da shi.

13 Mai albarka ne mutumin da ya sami hikima,
mutumin da ya sami fahimi,
14 gama ta fi azurfa riba
tana kuma da amfani fiye da zinariya.
15 Ta fi lu'ulu'u daraja;
ba a kwatanta abin da ka fi sha'awa da ita.
16 Tsawon rai yana a cikin hannunta na dama;
a hannunta na hagu kuwa akwai arziki da bangirma.
17 Hanyoyinta hanyoyi ne masu daɗi,
dukan hanyoyinta kuma salama ne.
18 Ita itacen rai ne ga waɗanda suka rungume ta;
waɗanda suke riƙe da ta za su zama masu albarka.

19 Ta wurin hikima UBANGIJI ya kafa harsashin duniya,
ta wurin fahimi ya shirya sammai inda suke;
20 ta wurin sani aka rarraba zurfafa,
gizagizai kuma suka zubo raɓa.

21 Ɗana, ka riƙe sahihiyar shari'a da kuma basira,
kada ka bar su su rabu da kai;
22 za su zama rai a gare ka,
abin adon da zai gyara wuyanka.
23 Sa'an nan za ka bi hanyarka lafiya,
ƙafarka kuwa ba zai yi tuntuɓe ba;
24 sa'ad da ka kwanta, ba za ka ji tsoro ba;
sa'ad da ka kwanta, barci zai yi maka daɗi.
25 Kada ka ji tsoron masifar da za tă faru farat ɗaya
ko lalacin da yakan auka wa mugaye,

* **3:6** Ko kuwa zai nuna maka hanyoyi

26 gama UBANGIJI zai zama ƙarfin halinka
zai kuwa kiyaye ƙafarka daga fāɗawa a tarko.

27 Kada ka ƙi yin alheri ga duk wanda ya dace,
sa'ad da kana iya yin haka.
28 Kada ka ce wa maƙwabcinka
"Ka yă dakata sai gobe,"
idan kana iya taimakonsa yanzu.
29 Kada ka shirya kome da zai cuci maƙwabcinka,
wanda yake zama da aminci kusa da kai.
30 Kada ka zargi mutum ba dalili,
sa'ad da bai yi laifi ba.

31 Kada ka ji kishin mai tā-da-na-zaune-tsaye
ko ka yi sha'awar aikata ayyukansu.

32 Gama UBANGIJI yana ƙyama mai aikata mugunta
amma yakan rungumi adalin da ya amince da shi.
33 La'anar UBANGIJI tana a gidan mugaye,
amma yakan albarkaci gidan adali.
34 Yakan yi wa masu girman kai ba'a
amma yakan yi wa mai sauƙinkai alheri.
35 Masu hikima sukan sami kyakkyawan suna,
amma wawaye sukan ƙara wa kansu shan kunya.

# 4

*Hikima ce mafi girma duka*

1 Ku saurara 'ya'yana ga koyarwar mahaifinku;
ku mai da hankali, ku sami fahimi.
2 Ina ba ku sahihiyar koyarwa,
saboda haka kada ku ƙyale koyarwata.
3 Sa'ad da nake yaro a gidan mahaifina,
yaro kaɗai kuma na mahaifiyata,
4 ya koya mini ya ce,
"Ka riƙe kalmomina da dukan zuciyarka;
ka kiyaye umarnaina za ka kuwa rayu.
5 Ka nemi hikima, ka nemi fahimi;
kada ka manta da kalmomina ko ka kauce daga gare su.
6 Kada ka ƙyale hikima, za tă kuwa tsare ka;
ka ƙaunace ta, za tă kuwa lura da kai.
7 Hikima ce mafi girma duka; saboda haka ka nemi hikima.
Ko da za tă ci duk abin da kake da shi, ka dai nemi fahimi.
8 Ka ƙaunace ta, za tă ɗaukaka ka;
ka rungume ta, za tă kuwa girmama ka.
9 Za tă zama kayan ado da za su inganta kanka
tă kuma zamar maka rawanin ɗaukaka."

10 Ka saurara, ɗana, ka yarda da abin da na faɗa,
shekarun rayuwarka kuwa za su zama masu yawa.
11 Na bishe ka a hanyar hikima

na kuma jagorance ka a miƙaƙƙun hanyoyi.
12 Sa’ad da kake tafiya, ba abin da zai sa ka tuntuɓe;
sa’ad da kake gudu, ba za ka fāɗi ba.
13 Ka riƙe umarni, kada ka bari yă kuɓuce;
ka tsare shi sosai, gama ranka ne.
14 Kada ka sa ƙafa a kan hanyar mugaye
kada ka bi gurbin mugaye.
15 Ka guji mugunta, kada ka yi tafiya a kanta;
juya daga gare ta ka yi tafiyarka.
16 Mugaye ba sa iya barci, sai sun aikata mugunta;
ba su barci sai sun cuci wani.
17 Mugunta da ta’adi
kamar ci da sha suke a gare su.

18 Hanyar adali kamar fitowar rana ce,
sai ƙara haske take yi, har ta kai tsaka.
19 Amma hanyar mugaye kamar zurfin duhu ne;
ba sa sanin abin da ya sa suke tuntuɓe.

20 Ɗana, ka kula da abin da nake faɗa,
ka saurara sosai ga kalmomina.
21 Kada ka bari su rabu da kai,
ka kiyaye su a cikin zuciyarka;
22 gama rai ne ga waɗanda suke nemansu
da kuma lafiya ga dukan jikin mutum.
23 Fiye da kome duka, ka tsare zuciyarka,
gama maɓulɓulan ruwan rijiyar rai ne.
24 Ka kau da muguwar magana daga bakinka;
ka yi nesa da magana marar kyau daga leɓunanka.
25 Bari idanunka su dubi gaba sosai,
ka kafa idanunka kai tsaye a gabanka.
26 Ka san inda ƙafafunka suke takawa
ka bi hanyoyin da suke daram kawai.
27 Kada ka kauce dama ko hagu;
ka kiyaye ƙafarka daga mugunta.

# 5

*Gargaɗi a kan zina*

1 Ɗana, ka mai da hankali ga hikimata
ka saurara da kyau ga kalmomin basirata,
2 don ka ci gaba da yin kome daidai
leɓunanka za su adana sani.
3 Gama leɓunan mazinaciya na ɗigan zuma,
maganarta tana da sulɓi fiye da mai;
4 amma a ƙarshe tana da ɗaci kamar tafashiya,
mai ci kamar takobi mai kaifi biyu.
5 Kafafunta na kaiwa ga mutuwa;
sawunta na jagora kai tsaye zuwa kabari.
6 Ba ta wani tunanin rayuwa;
hanyoyinta karkatacce ne, amma ba tă sani ba.

7 Yanzu fa, ’ya’yana, ku saurare ni;
kada ku juye daga abin da nake faɗa.
8 Ku yi nesa da hanyarta,
kana ku je kusa da ƙofar gidanta,
9 don kada ku ba da ƙarfi mafi kyau ga waɗansu
da kuma shekarunku ga wani marar imani,
10 don kada baƙi su yi biki a kan dukiyarku
wahalarku ta azurta gidan wani mutum dabam.
11 A ƙarshen rayuwarku za ku yi ta nishi,
sa’ad da namanku da jikinku suka zagwanye.
12 Za ku ce, “Me ya sa na ƙi horo!
Me ya sa zuciyata ta ƙi gyara!
13 Ban yi biyayya da malamaina ba
ko in saurari masu koyar da ni.
14 Na zo gab da hallaka gaba ɗaya
a tsakiyar dukan taron.”

15 Ku sha ruwa daga tankinku,
ruwa mai gudu daga rijiyarku.
16 In maɓulɓulanku suka cika suna malala har waje,
rafuffukan ruwanku a dandalin jama’a?
17 Bari su zama naka kaɗai,
don kada ka raba da baƙi.
18 Bari maɓulɓulanka ya zama mai albarka,
bari kuma ka yi farin ciki da matar ƙuruciyarka.
19 Kaunatacciyar mariri, barewa mai kyan gani,
bari mamanta su ishe ka kullum,
bari ƙaunarta ta ɗauke hankalinka kullum.
20 Ɗana, me ya sa za ka bari mazinaciya ta ɗauke maka hankali?
Don me za ka rungume matar wani?

21 Gama hanyar mutum a bayyane take a gaban UBANGIJI,
yana kuma lura da dukan hanyoyinsa.
22 Ayyukan mugunta na mugun mutum tarko ne gare shi;
igiyoyin zunubinsa za su daure shi kankan.
23 Zai mutu saboda rashin ɗa’a
yawan wawancinsa zai sa yă kauce.

# 6

*Gargaɗi a kan wawanci*

1 Ɗana, in ka shirya tsaya wa maƙwabcinka don yă karɓi bashi,
in ka sa hannunka don ɗaukar lamunin wani,
2 in maganarka ta taɓa kama ka,
ko kalmomin bakinka sun zama maka tarko,
3 to, sai ka yi haka, ɗana don ka ’yantar da kanka;
da yake ka shiga hannuwan maƙwabcinka,
ka tafi ka ƙasƙantar da kanka;
ka roƙi maƙwabcinka!
4 Ka hana kanka barci,
ko gyangyaɗi a idanunka ma.
5 Ka ’yantar da kanka, kamar barewa daga hannun mai farauta,

kamar tsuntsu daga tarkon mai kafa tarko.

6 Ku tafi wurin kyashi, ku ragwaye;
ku lura da hanyoyinsa ku zama masu hikima!
7 Ba shi da jagora
ba shugaba ko mai mulki,
8 duk da haka yakan yi tanade-tanadensa da rani
ya kuma tattara abincinsa a lokacin girbi.

9 Har yaushe za ku kwanta a can, ku ragwaye?
Yaushe za ku farka daga barcinku?
10 Ɗan barci, ɗan gyangyaɗi,
ɗan naɗin hannuwa don a huta,
11 talauci kuwa zai zo kamar ’yan hari
rashi kuma kamar ɗan fashi.

12 Sakare da mutumin banza
wanda yana yawo da magana banza a baki,
13 wanda yake ƙyifce da ido,
yana yi alama da ƙafafunsa
yana kuma nuni da yatsotsinsa,
14 wanda yake ƙulla mugunta da ruɗu a cikin zuciyarsa,
kullum yana tā-da-na-zaune-tsaye
15 Saboda haka masifa za tă fāɗa farat ɗaya;
za a hallaka shi nan da nan, ba makawa.

16 Akwai abubuwa shida da UBANGIJI ya ƙi,
abubuwa bakwai da suke abin ƙyama gare shi,
17 duban reni,
harshe mai ƙarya,
hannuwa masu zub da jinin marar laifi,
18 zuciyar da take ƙulla mugayen dabaru,
ƙafafun da suke sauri zuwa aikata mugunta,
19 mai shaidar ƙarya wanda yake zuba ƙarairayi,
da kuma mutumin da yake tā-da-na-zaune-tsaye a cikin ’yan’uwa.

### *Gargaɗi a kan zina*

20 Ɗana, ka kiyaye umarnan mahaifinka
kada kuma ka ƙyale koyarwar mahaifiyarka.
21 Ka ɗaura su a zuciyarka har abada;
ka ɗaura su kewaye da wuyanka.
22 Sa’ad da kake tafiya, za su bishe ka;
sa’ad da kake barci, za su lura da kai;
sa’ad da ka farka, za su yi maka magana.
23 Gama waɗannan umarnai fitila ne,
wannan koyarwa haske ne,
kuma gyare-gyaren horo
hanyar rayuwa ce,
24 suna kiyaye ka daga mace marar ɗa’a
daga sulɓin harshen mace marar aminci.

25 Kada ka yi sha’awarta a cikin zuciyarka
kada ka bar ta tă ɗauki hankalinka da idanunta.

26 Gama karuwa takan mai da kai kamar burodin kyauta,
mazinaciya kuma takan farauci ranka.
27 Mutum zai iya ɗiba wuta ya zuba a cinyarsa
ba tare da rigunansa sun ƙone ba?
28 Mutum zai iya yin tafi a garwashi wuta mai zafi
ba tare da ƙafafunsa sun ƙone ba?
29 Haka yake da wanda ya kwana da matar wani;
babu wanda ya taɓa ta da zai tafi babu hukunci.

30 Mutane ba sa ƙyale ɓarawo in ya yi sata
don yă ƙosar da yunwarsa sa’ad da yake jin yunwa.
31 Duk da haka in aka kama shi, dole yă biya sau bakwai
ko da yake abin zai ci dukan arzikin gidansa.
32 Amma mutumin da ya yi zina ba shi da hankali;
duk wanda ya yi haka yana hallaka kansa ne.
33 Dūka da kunya ne za su zama rabonsa,
kuma kunyarsa za tă dawwama.

34 Gama kishi kan tā da hasalar miji,
kuma ba zai ji tausayi ba sa’ad da yake ramawa.
35 Ba zai karɓi duk wata biya ba;
zai ƙi cin hanci, kome yawansu.

# 7

*Gargaɗi A kan mazinaciya*

1 Ɗana, ka kiyaye kalmomina
ka kuma ajiye umarnaina a cikinka.
2 Ka kiyaye umarnaina za ka kuwa rayu;
ka tsare koyarwata kamar ƙwayar idonka.
3 Ka daure su a yatsotsinka;
ka rubuta su a allon zuciyarka.
4 Ka faɗa wa hikima, “Ke ’yar’uwata ce,”
ka kuma kira fahimi danginka;
5 za su kiyaye ka daga mazinaciya,
daga mace marar aminci da kalmominta masu ɗaukan hankali.

6 A tagar gidana
na leƙa ta labule mai rammuka.
7 Sai na gani a cikin marasa azanci,
na lura a cikin samari,
wani matashi wanda ba shi da hankali.
8 Yana gangarawa a titi kusa da kusurwarta,
yana tafiya a gefen wajen gidanta
9 da magariba, yayinda rana tana fāɗuwa,
yayinda duhun dare yana farawa.

10 Sai ga mace ta fito don ta sadu da shi,
saye da riga kamar karuwa shirye kuma don ta yaudare shi.

11 (Ba ta jin tsoro, ko kuma kunya,
ƙafafunta ba sa zama a gida;
12 wani lokaci a titi, wani lokaci a dandali,
tana yawo a kowace kusurwa.)
13 Sai ta kama shi ta rungume shi
da duban soyayya a fuskarta ta ce,

14 "Ina da hadaya ta salama a gida;
yau zan cika alkawarina.
15 Saboda haka na fito don in sadu da kai;
na neme ka na kuma same ka!
16 Na lulluɓe gadona
da lili masu launi dabam-dabam daga Masar.
17 Na yayyafa turare a gadona
da mur, aloyes da kuma kirfa.
18 Zo, mu sha zurfin ƙauna har safe;
bari mu ji wa ranmu daɗi da ƙauna!
19 Mijina ba ya gida;
ya yi tafiya mai nisa.
20 Ya ɗauki jakarsa cike da kuɗi
ba zai kuwa dawo gida ba sai tsakiyar wata."

21 Da kalmomin rarrashi ta sa ya kauce;
ta ɗauki hankalinsa da sulɓin maganarta.
22 Nan take, ya bi ta
kamar saniyar da za a kai mayanka,
kamar wawa zuwa wurin da za a ba shi horo
23 sai da kibiya ta soki hantarsa,
kamar tsuntsun da ya ruga cikin tarko,
ba tare da sani zai zama sanadin ransa ba.

24 Yanzu fa, 'ya'yana, ku saurare ni;
ku kasa kunne ga abin da nake faɗa.
25 Kada ku bar zuciyarku ta juya zuwa hanyoyinta
ko ku kauce zuwa hanyoyinta.
26 Ta zama sanadin fāɗuwar yawanci;
kisan da ta yi ba ta ƙidayuwa.
27 Gidanta babbar hanya ce zuwa kabari
mai yin jagora zuwa ɗakunan lahira.

# 8

*Kiran hikima*

1 Hikima ba ta yin kira ne?
Fahimi ba ya tā da muryarsa ne?
2 A ƙwanƙoli a kan hanya,
inda hanyoyi suka haɗu, ta ɗauki matsayinta;
3 kusa da ƙofofin shiga cikin birni,
a mashigai, ta tā da murya,
4 "Gare ku, ya mutane, nake kira;
na tā da muryata ga dukan 'yan adam.
5 Ku da kuke marasa azanci, ku yi hankali;

ku da kuke wawaye, ku nemi fahimi.
6 Ku saurara, gama ina da abubuwa masu darajan da zan faɗa;
na buɗe leɓunana don in faɗa abin da yake daidai.
7 Bakina yana magana abin da yake gaskiya,
gama leɓunana sun ƙi mugunta.
8 Dukan kalmomin bakina suna da adalci;
babu waninsu da ya karkace ko kuwa ƙarya ne.
9 Ga mai tunani dukansu daidai ne;
ba su da laifi ga waɗanda suke da sani.
10 Ku zaɓi umarnina a maimakon azurfa,
sani a maimakon zinariya zalla,
11 gama hikima ta fi lu'ulu'ai daraja,
kuma ba abin da kake sha'awa da za a kwatanta da ita.

12 "Ni, hikima, ina zama tare da hankali;
ina da sani da iya rarrabewa.
13 Jin tsoron Ubangiji shi ne ƙin mugunta;
ina ƙin girman kai da fariya,
halin mugunta da kuma muguwar magana.
14 Shawara da yin tunani mai kyau nawa ne;
ina da fahimi da kuma iko.
15 Ta wurina sarakuna suke mulki
masu mulki kuma suke yin dokokin da suke da adalci;
16 ta wurina sarakuna suke mulki,
da kuma dukan manyan mutanen da suke mulkin duniya.
17 Ina ƙaunar waɗanda suke ƙaunata,
kuma waɗanda suke nemana sukan same ni.
18 Tare da ni akwai wadata da girmamawa,
dukiya da wadata masu dawwama.
19 'Ya'yan itacena sun fi zinariya zalla;
amfanin gonar da nake bayar ya fi azurfa mafi kyau.
20 Ina tafiya a hanyar adalci,
a kan hanyoyin gaskiya,
21 ina ba da wadata ga waɗanda suke ƙaunata
ina sa wuraren ajiyarsu su cika.

22 "Ubangiji ya kawo ni a matsayi na farko na ayyukansa,
kafin ayyukansa na tuntuni;
23 an naɗa ni tun fil azal,
daga farko, kafin duniya ta kasance.
24 Sa'ad da babu tekuna, aka haife ni,
sa'ad da babu maɓulɓulai masu ruwa;
25 kafin a kafa duwatsu a wurarensu,
kafin tuddai ma, an haife ni,
26 kafin ya yi duniya ko gonaki
ko wata ƙurar duniya.
27 Ina nan sa'ad da ya kafa sammai a wurarensu,
sa'ad da ya shata sararin sama a kan fuskar zurfafa,
28 sa'ad da ya kafa gizagizai a bisa
ya kuma kafa maɓulɓulan zurfafa daram,
29 sa'ad da ya ba wa teku iyakarsa

domin kada ruwaye su zarce umarninsa,
da kuma sa'ad da ya shata tussan duniya.
30 A lokacin ni ne mai tsara abubuwa a gefensa.
Na cika da murna kowace rana,
kullum ina farin ciki a gabansa,
31 ina farin ciki da dukan duniyarsa
ina murna da 'yan adam.

32 "Yanzu fa, 'ya'yana, ku saurare ni;
masu albarka ne waɗanda suke kiyaye hanyoyina.
33 Ku saurari umarnina ku kuma zama masu hikima;
kada ku ƙyale ta.
34 Mai albarka ne wanda ya saurare ni;
yana tsaro kullum a ƙofofina,
yana jira a ƙofar shigata.
35 Gama duk wanda ya same ni ya sami rai
zai kuma sami tagomashi daga UBANGIJI.
36 Amma duk wanda ya kāsa samuna ya cuci kansa;
dukan waɗanda suke ƙina suna ƙaunar mutuwa ke nan."

# 9

*Gayyatar hikima da gayyatar wawanci*

1 Hikima ta gina gidanta;
ta yi ginshiƙansa bakwai.
2 Ta shirya abincinta gauraye da ruwan inabinta;
ta kuma shirya teburinta.
3 Ta aiki bayinta mata, tana kuma kira
daga wurare masu tsayi na birnin.
4 "Bari dukan waɗanda suke marasa azanci su zo nan ciki!"
Tana faɗa wa marasa hankali.
5 "Ku zo, ku ci abincina
da ruwan inabin da na gauraye.
6 Ku bar hanyoyinku marasa hankali za ku kuwa rayu;
yi tafiya a hanyar fahimi.

7 "Duk wanda ya yi wa mai ba'a gyara yana gayyatar zagi
duk wanda ya tsawata wa mugu yakan gamu da cin mutunci.
8 Kada ka tsawata wa masu ba'a gama za su ƙi ka;
ka tsawata wa mai hikima zai kuwa ƙaunace ka.
9 Ka koya wa mai hikima zai kuwa ƙara hikima;
ka koya wa mai adalci zai kuwa ƙara koyonsa.

10 "Tsoron UBANGIJI shi ne mafarin hikima,
sanin Mai Tsarki kuwa fahimi ne.
11 Gama ta wurina kwanakinka za su yi yawa,
za a kuwa ƙara wa ranka shekaru.
12 In kana da hikima, hikimarka za tă ba ka lada;
in kai mai ba'a ne, kai kaɗai za ka sha wahala."

13 Wawancin mace a bayyane yake;
ba ta da ɗa'a kuma ba ta da sani.

14 Takan zauna a ƙofar gidanta,
a wurin zama a wurin mafi tsayi na birni,
15 tana kira ga masu wucewa,
waɗanda suke tafiya kai tsaye a hanyarsu.
16 “Bari dukan waɗanda suke marasa azanci su zo cikin nan!”
Tana ce wa marasa hankali.
17 “Ruwan da aka sata ya fi daɗi;
abincin da aka ci a ɓoye ya fi daɗi!”
18 Amma ba su san cewa matattu suna a can ba,
cewa baƙinta suna a can cikin zurfin kabari ba.

# Karin maganar Solomon

## 10

1 Karin maganar Solomon.
Ɗa mai hikima yakan kawo wa mahaifinsa farin ciki,
amma wawan ɗa kan sa wa mahaifiyarsa baƙin ciki.

2 Dukiyar da aka samu a hanyar da ba tă dace ba, ba ta da albarka,
amma adalci kan ceci mutum daga mutuwa.

3 Ubangiji ba ya barin mai adalci da yunwa
amma yakan lalace burin mugu.

4 Ragwanci kan sa mutum yă zama matalauci,
amma aiki tuƙuru kan ba da dukiya.

5 Shi da ya tattara hatsi da rani ɗa ne mai hikima,
amma shi da yakan yi barci a lokacin girbi ɗa ne wanda ya zama abin kunya.

6 Albarka kan zauna a kan mai adalci kamar rawani,
amma rikici kan sha bakin mugu.

7 Tunawa da mai adalci albarka ne
amma sunan mugu zai ruɓe.

8 Mai hikima a zuciya yakan yarda da umarni
amma surutun wawa kan kai ga lalaci.

9 Mai mutunci yana tafiya lafiya,
amma shi da yake tafiya a karkatattun hanyoyi za a kama shi.

10 Shi da ya ƙyifta ido da mugunta kan jawo baƙin ciki
surutun wawa kuma kan zo da lalaci.

11 Bakin adali maɓulɓulan rai ne,
amma kalmar mugun takan ɓoye makircinsa.

12 Kiyayya kan haddasa wahala,
amma ƙauna kan rufe dukan laifofi.

13 Ana samun hikima a leɓunan masu fahimi,
amma bulala domin bayan marasa azanci ne.

14 Mai hikima kan yi ajiyar sani,
amma bakin wawa kan gayyaci lalaci.

15 Dukiyar masu arziki yakan zama mafakar birninsu,
amma talauci shi ne lalacin matalauci.

16 Hakkin adalai kan kawo musu rai,
amma albashin mugaye kan kawo musu hukunci.

17 Duk wanda ya mai da hankali ga horo kan nuna hanyar rai,
amma duk wanda ya ƙyale gyara kan sa waɗansu su kauce.

18 Duk wanda ya ɓoye ƙiyayyarsa yana da ƙarya a leɓunansa,
duk kuma wanda yake baza ƙarairayi wawa ne.

19 Sa'ad da magana ta yi yawa, ba a rasa zunubi a ciki,
amma shi da ya ƙame harshensa mai hikima ne.

20 Harshen adali azurfa ce zalla,
amma zuciyar mugu ba ta da wani amfani.

21 Leɓunan adalai kan amfane yawanci,
amma wawa kan mutu saboda rashin azanci.

22 Albarkar UBANGIJI kan kawo wadata,
ba ya kuma ƙara wahala a kai.

23 Wawa yakan ji daɗi halin mugunta,
amma mutum mai fahimi kan ji daɗin hikima.

24 Abin da mugu ke tsoro shi ne zai same shi;
abin da adali ke bukata yakan sami biyan bukata.

25 Sa'ad da hadiri ya taso, yakan watsar da mugaye,
amma adalai za su tsaya daram har abada.

26 Kamar yadda ruwan tsami yake ga haƙora hayaƙi kuma ga idanu,
haka malalaci yake ga wanda ya aike shi.

27 Tsoron UBANGIJI kan ƙara tsawon rai,
amma akan gajartar da shekarun mugaye.

28 Abin da adali yake sa rai yakan kai ga farin ciki,
amma sa zuciyar mugu ba ya haifar da kome.

29 Hanyar UBANGIJI mafaka ce ga adalai
amma lalaci ne ga waɗanda suke aikata mugunta.

30 Ba za a taɓa tumɓuke masu adalci ba,
amma mugaye ba za su ci gaba da kasance a ƙasar ba.

31 Bakin adalai kan fitar da hikima,
amma za a dakatar da mugun harshe.

32 Leɓunan adalai sun san abin da ya dace,
amma bakunan mugaye sun san abin da yake mugu ne kawai.

## 11

1 UBANGIJI yana ƙyamar ma'aunan zamba,
amma ma'aunin da suke daidai ne abin farin cikinsa.

2 Sa'ad da girman kai ya zo, sai shan kunya ta zo,
amma hikima kan zo tare da ƙasƙantar da kai.

3 Mutuncin masu aikata gaskiya takan bi da su,
amma marasa aminci sukan hallaka ta wurin cin amanar da suke yi.

4 Dukiya ba ta da amfani a ranar fushi,
amma adalci kan yi ceto daga mutuwa.

5 Adalcin marasa laifi kan miƙe hanyarsu,
amma akan ƙasƙantar da mugaye ta wurin muguntarsu.

6 Adalcin masu aikata gaskiya kan cece su,
amma rashin aminci tarko ne ga mugayen sha'awace-sha'awace.

7 Sa'ad da mugu ya mutu, sa zuciyarsa kan hallaka;
dukan abin da ya sa zuciya daga ikonsa ba ya amfana kome.

8 Akan kuɓutar da mai adalci daga wahala,
sai ta dawo wa mugu a maimako.

9 Da bakinsa marar sanin Allah kan hallaka maƙwabcinsa,
amma ta wurin sani mai adalci kan kuɓuta.

10 Sa'ad da adali ya yi nasara, birnin kan yi farin ciki;
sa'ad da mugu ya hallaka, akwai sowa ta farin ciki.

11 Ta wurin albarkar mai aikata gaskiya birni kan ƙasaita,
amma ta wurin bakin mugu akan hallaka birnin.

12 Mutum da ba shi da azanci kan ki maƙwabci,
amma mutum mai fahimi kan ƙame harshensa.

13 Gulma yakan lalace yarda,
amma mutum mai aminci kan kiyaye asiri.

14 Saboda rashin jagora al'umma takan fāɗi,
amma masu ba da shawara da yawa kan tabbatar da nasara.

15 Duk wanda ya ɗauki lamunin wani tabbatacce zai sha wahala,
amma duk wanda ya ƙi ya sa hannu a ɗaukar lamuni ba ruwansa.

16 Mace mai hankali na samu bangirma,
amma azzalumai za su sami dukiya.

17 Mutumin kirki kan ribance kansa,
amma mugu kan kawo wa kansa wahala.

18 Mugun mutum kan sami albashin ƙarya
amma shi da ya shuka adalci zai girbe lada tabbatacce.

19 Mutum mai adalci da gaske yakan sami rai,
amma shi da ya duƙufa ga aikata mugunta kan tarar da mutuwarsa.

20 Ubangiji yana ƙyamar mutane masu muguwar zuciya
amma yana jin daɗin waɗanda hanyoyinsu ba su da laifi.

21 Ka tabbata da wannan. Mugaye ba za su tafi babu hukunci ba,
amma waɗanda suke masu adalci za su tafi babu hukunci.

22 Kamar zinariya a hancin alade
haka kyan mace wadda ba ta da hankali.

23 Sha'awar adalai kan ƙare kawai a aikata alheri,
amma sa zuciyar mugaye kan ƙarasa kawai a fushi.

24 Wani mutum kan bayar hannu sake, duk da haka yakan sami fiye;
wani yakan riƙe abin da ba nasa ba, amma sai ya ƙarasa cikin talauci.

25 Mutum mai kyauta zai azurta;
shi da yakan taimake waɗansu, za a taimake shi.

26 Mutane kan la'anci mai ɓoye hatsi yana jira ya yi tsada,
amma albarka kan zauna a kan wanda yake niyya ya sayar.

27 Duk mai nema alheri kan sami alheri,
amma mugu kan zo wa wanda yake nemansa.

28 Duk wanda ya dogara ga arzikinsa zai fāɗi,
amma adali zai yi nasara kamar koren ganye.

29 Duk wanda ya kawo wahala wa iyalinsa zai gāji iska kawai,
kuma wawa zai zama bawan masu hikima.

30 'Ya'yan itacen adali itacen rai ne,
kuma duk mai samun rayuka mai hikima ne.

31 In masu adalci sun sami abin da ya dace da su a duniya,
yaya zai zama ga marasa sanin Allah da kuma masu zunubi!

# 12

1 Duk mai ƙaunar horo yana ƙaunar sani,

amma duk mai ƙin gyara wawa ne.

2 Mutumin kirki kan sami tagomashi daga UBANGIJI,
amma UBANGIJI yakan hukunta mai son yin wayo.

3 Ba yadda mutum zai kahu ta wurin aikata mugunta,
amma ba za a tumɓuke adali ba.

4 Mace mai halin kirki rawanin mijinta ne,
amma mace marar kunya tana kama da ciwo a ƙasusuwansa.

5 Shirye-shiryen masu adalci daidai ne,
amma shawarar mugaye ruɗu ne.

6 Kalmomin mugu sukan kwanta suna jira su yi kisankai,
amma jawabin masu aikata gaskiya kan kuɓutar da su.

7 Akan tumɓuke mugaye ba a ƙara ganinsu,
amma gidan masu adalci kan tsaya daram.

8 Akan yabi mutum bisa ga hikimarsa,
amma mutane marasa azanci akan rena su.

9 Gara ka zama kai ba kome ba ne amma kana da bawa
da ka mai da kanka kai wani ne alhali kuwa ba ka da abinci.

10 Mai adalci kan kula da bukatun dabbobinsa,
amma halaye mafi kyau na mugaye su ne ƙeta.

11 Duk wanda ya nome gonarsa zai sami abinci a yalwace,
amma shi da yake naushin iska marar azanci ne.

12 Mugaye suna sha'awar ganimar mugayen mutane,
amma saiwar masu adalci kan haɓaka.

13 Mugun mutum kan fāɗa a tarkon maganarsa ta zunubi,
amma adali kan kuɓuta daga wahala.

14 Daga abubuwan da suke fitowa daga leɓunansa mutum kan cika da abubuwa masu kyau
tabbatacce yadda aikin hannuwansa suke ba shi lada.

15 Hanyar wawa daidai take a gare shi,
amma mai hikima kan saurari shawara.

16 Wawa kan nuna fushinsa nan take,
amma mai la'akari kan ƙyale zargi.

17 Mashaidin gaskiya kan ba da shaidar gaskiya,
amma mashaidin ƙarya yana baza ƙarairayi ne.

18 Maganganun rashin tunani sukan soki mutum kamar takobi,

amma harshen mai hikima kan kawo warkarwa.

19 Leɓunan gaskiya kan dawwama har abada,
amma harshen ƙarya yakan dawwama na ɗan lokaci ne kawai.

20 Akwai ruɗu a zukatan waɗanda suke ƙulla mugunta,
amma waɗanda suke aikata alheri za su yi farin ciki.

21 Ba wani lahanin da zai sami masu adalci,
amma mugaye suna da nasu cike da wahala.

22 UBANGIJI yana ƙyamar leɓunan masu ƙarya,
amma yana jin daɗin mutanen da suke masu gaskiya.

23 Mai la'akari kan kiyaye saninsa wa kansa,
amma zuciyar wawa kan yi ta tallar wawanci.

24 Hannuwan masu aiki tuƙuru za su yi mulki,
amma ragwanci kan ƙarasa a aikin bauta.

25 Zuciya mai damuwa takan naƙasar da mutum,
amma maganar alheri kan faranta masa rai.

26 Adali yakan yi hankali a abokantaka,
amma hanyar mugaye kan kai su ga kaucewa.

27 Rago ba ya gashin abin da ya kama daga farauta,
amma mai aiki tuƙuru yakan ɗauki mallakarsa da muhimmanci.

28 A hanyar adalci akwai rai;
a wannan hanya akwai rashin mutuwa.

# 13

1 Ɗa mai hikima yakan mai da hankali ga umarnin mahaifinsa,
amma mai ba'a ba ya sauraran kwaɓi.

2 Daga abin da ya fito leɓunan mutum ne mutum kan ji daɗin abubuwa masu kyau,
amma marar aminci yakan ƙosa ya tā-da-na-zaune-tsaye.

3 Duk mai lura da leɓunansa yakan lura da ransa,
amma duk mai magana da haushi zai kai ga lalaci.

4 Rago ya ƙosa ya sami wani abu ainun amma ba ya samun kome,
amma sha'awar mai aiki tuƙuru yakan ƙoshi sosai.

5 Adali yana ƙin abin da yake ƙarya,
amma mugu kan jawo kunya da ƙasƙanci.

6 Adalci yakan lura da mutum mai mutunci,
amma mugunta takan sha kan mai zunubi.

7 Wani mutum yakan ɗauki kansa mai arziki ne, alhali ba shi da kome,
wani ya ɗauki kansa shi matalauci ne, alhali shi mawadaci ne ƙwarai.

8 Arzikin mutum zai iya kuɓutar da ransa,
amma matalauci ba ya jin barazana.

9 Hasken masu adalci kan haskaka ƙwarai,
amma fitilar mugaye mutuwa take.

10 Girmankai kan jawo faɗa ne kawai,
amma hikima tana samuwa a waɗanda suke jin shawara.

11 Kuɗin da aka same su a rashin gaskiya yakan ɓace da sauri,
amma duk wanda ya tara kuɗi kaɗan-kaɗan za su yi ta ƙaruwa.

12 Sa zuciyar da aka ɗaga zuwa gaba kan sa zuciya tă yi ciwo,
amma marmarin da aka ƙosar yana kamar itacen rai.

13 Duk wanda ya rena umarni zai ɗanɗana ƙodarsa,
amma duk wanda ya yi biyayya da umarni zai sami lada.

14 Koyarwar mai hikima maɓulɓulan rai ne,
mai juyar da mutum daga tarkon mutuwa.

15 Fahimta mai kyau kan sami tagomashi,
amma hanyar marar aminci tana da wuya.

16 Kowane mai azanci yakan nuna sani,
amma wawa yakan yi tallen wawancinsa.

17 Mugun ɗan saƙo kan shiga wahala,
amma jakadan da mai aminci yakan kawo warkarwa.

18 Duk wanda ya ƙyale horo yakan kai ga talauci da kuma kunya,
amma duk wanda ya karɓi gyara yakan sami girma.

19 Marmarin da aka cika yana da daɗi ga rai,
amma wawa yana ƙyamar juyewa daga mugunta.

20 Shi da yake tafiya tare da masu hikima yakan ƙaru da hikima,
amma abokin wawaye zai yi fama da lahani.

21 Rashin sa'a kan fafare mai zunubi,
amma wadata ce ladar adali.

22 Mutumin kirki kan bar gādo wa 'ya'ya 'ya'yansa,
amma arzikin mai zunubi ajiye ne da aka yi wa mai adalci.

23 Gonar matalauci za tă iya ba da abinci a yalwace,
amma rashin adalci kan share shi tas.

24 Duk wanda ba ya horon ɗansa ba ƙaunarsa yake yi ba,
amma duk mai ƙaunarsa yakan kula ya hore shi.

25 Masu adalci sukan ci isashen abinci,
amma cikin mugaye na fama da yunwa.

# 14

1 Mace mai hikima kan gina gidanta,
amma da hannunta wawiya takan rushe shi ƙasa.

2 Wanda tafiyarsa ta aikata gaskiya ce kan ji tsoron UBANGIJI,
amma wanda hanyoyinsa ba a kan gaskiya ba ne yakan rena shi.

3 Maganar wawa kan kawo sanda a bayansa,
amma leɓunan masu hikima kan tsare su.

4 Inda ba shanu, wurin sa wa dabbobi abinci zai kasance ba kome,
amma daga ƙarfin saniya ce yalwar girbi kan fito.

5 Mashaidi na gaskiya ba ya ruɗu,
amma mashaidin ƙarya kan baza ƙarairayi.

6 Mai ba'a kan nemi hikima amma ba ya samun kome,
amma sani kan zo a sawwaƙe ga mai basira.

7 Ka guji wawa,
gama ba za ka sami sani a leɓunansa ba.

8 Hikima masu la'akari shi ne su yi tunani a kan hanyoyinsu,
amma wautar wawaye ruɗu ne.

9 Wawaye kan yi ba'a a gyaran zunubi,
amma fatan alheri yana samuwa a cikin masu aikata gaskiya.

10 Kowace zuciya ta san ɓacin ranta,
kuma babu wani dabam da zai yi rabon jin daɗinsa.

11 Za a rushe gidan mugu,
amma tentin mai aikata gaskiya zai haɓaka.

12 Akwai hanyar da ta yi kamar tana daidai ga mutum,
amma a ƙarshe takan kai ga mutuwa.

13 Ko cikin dariya zuciya takan yi ciwo,
kuma farin ciki kan iya ƙarasa a baƙin ciki.

14 Marasa bangaskiya za su sami sakamako cikakke saboda hanyoyinsu,
kuma mutumin kirki zai sami lada saboda nasa.

15 Marar azanci kan gaskata kome,

amma mai la'akari kan yi tunani game da matakinsa.

16 Mai hikima kan ji tsoron UBANGIJI ya kuma guji mugunta,
amma wawa yana da girman kai yakan yi kome da garaje.

17 Mutum mai saurin fushi yakan yi ayyukan wauta,
akan kuma ƙi mai son nuna wayo.

18 Marar azanci kan gāji wauta,
amma mai la'akari kan sami rawanin sani.

19 Masu mugunta za su rusuna a gaban masu kirki,
mugaye kuma za su yi haka a ƙofofin adalai.

20 Maƙwabta sukan gudu daga matalauta,
amma masu arziki suna da abokai da yawa.

21 Duk wanda ya rena maƙwabci ya yi zunubi,
amma mai albarka ne wanda yake alheri ga mabukata.

22 Ba waɗanda suke ƙulla mugunta sukan kauce ba?
Amma waɗanda suke ƙulla abin da yake mai kyau sukan sami ƙauna da aminci.

23 Duk aiki tuƙuru yakan kawo riba,
amma zama kana surutu kan kai ga talauci kawai.

24 Dukiyar masu hikima ita ce rawaninsu,
amma wautar wawaye kan haifar da wauta ne kawai.

25 Mashaidin gaskiya kan ceci rayuka,
amma mashaidin ƙarya mai ruɗu ne.

26 Duk mai tsoron UBANGIJI yana da zaunannen mafaka,
kuma ga 'ya'yansa zai zama mafaka.

27 Tsoron UBANGIJI shi ne maɓulɓular rai
yakan juye mutum daga tarkon mutuwa.

28 Yawan mutane shi ne ɗaukakar sarki,
amma in ba tare da mabiya ba sarki ba kome ba ne.

29 Mutum mai haƙuri yana da fahimi mai yawa,
amma mai saurin fushi yakan nuna wautarsa a fili.

30 Zuciya mai salama kan ba jiki rai,
amma kishi kan sa ƙasusuwa su yi ciwo.

31 Duk wanda ya zalunci matalauci ya zagi Mahaliccinsu ke nan,
amma duk wanda ya yi alheri ga mabukata yana girmama Allah ne.

32 Sa'ad bala'i ya auku, mugaye kan fāɗi,

amma ko a mutuwa masu adalci suna da mafaka.

33 Hikima tana a zuciyar mai azanci,
kuma ko a cikin wawaye takan sa a santa.

34 Adalci yakan ɗaukaka al’umma,
amma zunubi kan kawo kunya ga kowane mutane.

35 Sarki yakan yi murna a kan bawa mai hikima,
amma bawa marar kunya kan jawo fushinsa.

# 15

1 Amsa da tattausar harshe kan kwantar da fushi,
amma magana da kakkausan harshe kan kuta fushi.

2 Harshen mai hikima kan yi zance mai kyau a kan sani,
amma bakin wawa kan fitar da wauta.

3 Idanun UBANGIJI suna a ko’ina,
suna lura da masu aikata mugunta da masu aikata alheri.

4 Harshen da ya kawo warkarwa shi ne itacen rai,
amma harshe mai ƙarya kan ragargaza zuciya.

5 Wawa yakan ƙi kulawa da horon da mahaifinsa yake masa,
amma duk wanda ya yarda da gyara kan nuna azanci.

6 Gidan adali yana da dukiya mai yawa,
amma albashin mugaye kan kawo musu wahala.

7 Leɓunan masu hikima sukan baza sani;
ba haka zukatan wawaye suke ba.

8 UBANGIJI yana ƙyamar hadayar mugaye,
amma addu’ar masu aikata gaskiya kan sa ya ji daɗi.

9 UBANGIJI yana ƙin hanyar mugaye
amma yana ƙaunar waɗanda suke neman adalci.

10 Horo mai tsanani yana jiran duk wanda ya bar hanya;
wanda ya ƙi gyara zai mutu.

11 Mutuwa da Hallaka suna nan a fili a gaban UBANGIJI,
balle fa zukatan mutane!

12 Mai yin ba’a yakan ƙi gyara;
ba zai nemi shawara mai hikima ba.

13 Zuciya mai farin ciki kan sa fuska tă yi haske,
amma ciwon zuciya kan ragargaza rai.

14 Zuciya mai la’akari kan nemi sani,
amma bakin wawa wauta ce ke ciyar da shi.

15 Dukan kwanakin mutumin da ake danniya fama yake yi,
amma zuciya mai farin ciki yana yin biki kullum.

16 Gara a kasance da kaɗan da tsoron UBANGIJI
da a kasance da arziki mai yawa game da wahala.

17 Gara a ci abincin kayan ganye inda akwai ƙauna
da a ci kiwotaccen saniya inda ƙiyayya take.

18 Mutum mai zafin rai kan kawo faɗa,
amma mutum mai haƙuri kan kwantar da faɗa.

19 An tare hanyar rago da ƙayayyuwa,
amma hanyar mai aikata gaskiya buɗaɗɗiyar hanya ce.

20 Ɗa mai hikima kan kawo farin ciki wa mahaifinsa,
amma wawa yakan rena mahaifiyarsa.

21 Wauta kan sa mutum marar azanci ya yi farin ciki,
amma mai basira kan kiyaye abin da yake yi daidai.

22 Shirye-shirye sukan lalace saboda rashin neman shawara,
amma tare da mashawarta masu yawa za su yi nasara.

23 Mutum yakan yi farin ciki a ba da amsar da take daidai,
kuma ina misali a yi magana a lokacin da ya dace!

24 Hanyar rai na yin jagora ya haura wa masu hikima
don ta kiyaye shi daga gangarawa zuwa kabari.

25 UBANGIJI yakan rushe gidan mai girman kai
amma yakan kiyaye iyakokin gwauruwa daidai.

26 UBANGIJI yana ƙyamar tunanin mugaye,
amma waɗanda suke da tunani masu tsabta yakan ji daɗinsu.

27 Mutum mai haɗama kan kawo wahala ga iyalinsa,
amma wanda yake ƙin cin hanci zai rayu.

28 Zuciyar mai adalci takan auna amsoshinta,
amma bakin mugu yakan fitar da mugunta.

29 UBANGIJI yana nesa da mugaye
amma yakan ji addu’ar adalai.

30 Fuska mai fara’a takan kawo farin ciki ga zuciya,
kuma labari mai daɗi na kawo lafiya ga ƙasusuwa.

31 Duk wanda ya mai da hankali sa’ad da ake tsawata masa
ba zai kasance dabam a cikin masu hikima ba.

32 Duk waɗanda suka ƙi horon sun rena kansu ke nan,
amma duk waɗanda sun yarda da gyara sukan ƙara basira.

33 Tsoron Ubangiji yakan koya wa mutum hikima,
kuma sauƙinkai kan zo kafin girmamawa.

# 16

1 Ga mutum ne shirye-shiryen zuciya suke,
amma daga Ubangiji ne amshin harshe kan zo.

2 Dukan hanyoyin mutum sukan yi kamar marar laifi ne gare shi,
amma Ubangiji yakan auna manufofi.

3 Ka miƙa wa Ubangiji dukan abin da kake yi,
shirye-shiryenka kuwa za su yi nasara.

4 Ubangiji yana yin kome domin amfaninsa,
har ma da mugaye domin ranar masifa.

5 Ubangiji yana ƙyamar dukan zuciya mai girman kai.
Ka tabbata da wannan. Ba za su kuɓuta daga hukunci ba.

6 Ta wurin ƙauna da aminci akan yi kafarar zunubi;
ta wurin tsoron Ubangiji mutum kan guji mugunta.

7 Sa’ad da hanyoyin mutum sun gamshi Ubangiji,
yakan sa abokan gāban mutumin ma su zauna lafiya da shi.

8 Gara ka sami kaɗan ta hanyar adalci
da sami riba mai yawa ta hanyar rashin gaskiya.

9 ’Yan Adam sukan yi shirye-shiryensu a zukatansu,
amma Ubangiji ne yake da ikon cika matakansa.

10 Leɓunan sarki kan yi magana kamar ta wurin ikon Allah,
kuma bai kamata bakinsa ya yi kuskure a yanke shari’a ba.

11 Ma’aunai da magwajin gaskiya daga Ubangiji ne;
dukan ma’aunai da suke cikin jaka yinsa ne.

12 Sarakuna suna ƙyamar abin da ba shi da kyau,
gama an kafa kujerar sarauta ta wurin adalci ne.

13 Sarakuna sukan ji daɗi leɓuna masu yin gaskiya;
sukan darjanta mutumin da yake faɗin gaskiya.

14 Fushin sarki ɗan saƙon mutuwa ne,

amma mai hikima yakan faranta masa rai.

15 Sa'ad da fuskar sarki ta haska, yana nufin rai ke nan;
tagomashinsa yana kamar girgijen ruwa a bazara.

16 Ya ma fi kyau ka sami hikima fiye da zinariya,
ka zaɓi fahimi a maimakon azurfa!

17 Buɗaɗɗiyar hanyar masu aikata gaskiya kan guje wa mugunta;
duk wanda yake lura da hanyarsa yakan lura da ransa.

18 Girmankai yakan zo kafin hallaka,
girman kai yakan zo kafin fāɗuwa.

19 Gara ka zama ɗaya daga cikin matalauta masu sauƙinkai,
da ka raba ganima da masu girman kai.

20 Duk wanda ya mai da hankali ga umarni yakan yi nasara,
kuma mai albarka ne wanda yake dogara ga Ubangiji.

21 Akan ce da masu hikima a zuciya hazikai,
kuma kalmomi masu daɗi kan inganta umarni.

22 Fahimi shi ne maɓulɓular rai ga waɗanda suke da shi,
amma wauta kan kawo hukunci ga wawaye.

23 Zuciyar mai hikima kan bi da bakinsa,
kuma leɓunansa kan inganta umarni.

24 Kalmomi masu daɗi suna kama da kakin zuma,
mai zaƙi ga rai da kuma warkarwa ga ƙasusuwa.

25 Akwai hanyar da ta yi kamar daidai ga mutum,
amma a ƙarshe takan kai ga mutuwa.

26 Marmarin cin abinci yakan yi wa ɗan ƙodago aiki;
yunwarsa kan sa ya ci gaba.

27 Mutumin banza yakan ƙulla mugunta,
kuma jawabinsa yana kama da wuta mai ƙuna.

28 Fitinannen mutum yakan zuga tashin hankali,
mai gulma kuma yakan raba abokai na kusa.

29 Mutum mai tā-da-na-zaune-tsaye yakan ruɗi maƙwabcinsa
ya kai shi a hanyar da ba ta da kyau.

30 Duk wanda ya ƙyifce da idonsa yana ƙulla maƙarƙashiya ce;
duk wanda ya murguɗa leɓunansa yana niyya aikata mugunta ke nan.

31 Furfura rawani ne mai daraja;

akan same ta ta wurin yin rayuwa ta adalci.

32 Gara ka zama mai haƙuri da ka zama jarumi,
ya fi kyau ka iya mallakar kanka fiye da mallakar birane.

33 Akan jefa ƙuri'a a kan cinya,
amma kowace shawara mai kyau daga UBANGIJI ne.

# 17

1 Gara ka ci busasshen burodi da kwanciyar rai kuma shiru
da ka je cin abinci a gidan da ke cike da biki amma da ɓacin rai.

2 Bawa mai hikima zai yi mulki a kan da mai rashin kunya,
kuma zai raba gādo kamar ɗaya daga cikin 'yan'uwansa.

3 Ana gwajin azurfa da kuma zinariya da wuta,
amma UBANGIJI ne mai gwajin zuciya.

4 Mugun mutum kan mai da hankali ga mugayen leɓuna;
maƙaryaci yakan kasa kunne ga harshen ƙarairayi.

5 Duk wanda yake wa matalauta ba'a yana zagin Mahaliccinsu ne;
duk wanda ya yi murna akan masifar da ta sami wani za a hukunta shi.

6 Jikoki rawanin tsofaffi ne,
kuma iyaye su ne abin taƙamar 'ya'yansu.

7 Leɓunan basira ba su dace da wawa ba,
ya ma fi muni a ce mai mulki yana da leɓunan ƙarya!

8 Cin hanci kamar sihiri yake ga wanda yake ba da shi;
ko'ina ya juye, yakan yi nasara.

9 Duk wanda ya rufe laifi yana inganta ƙauna ne,
amma duk wanda ya yi ta maimaita batu yakan raba abokai na kusa.

10 Tsawata kan sa mutum ya koyi basira
fiye da abin da wawa zai koya ko da an dūke shi sau ɗari.

11 Mugayen mutane sukan kuta tawaye da Allah;
za a aika manzo mutuwa a kansu.

12 Gara a haɗu da beyar da aka ƙwace wa 'ya'ya
fiye da a sadu da wawa cikin wautarsa.

13 In mutum ya sāka alheri da mugunta,
mugunta ba za tă taɓa barin gidansa ba.

14 Farawar faɗa tana kamar ɓarkewa madatsar ruwa ne,
saboda haka ka bar batun kafin faɗa ta ɓarke.

15 Baratar da mai laifi a kuma hukunta mai adalci,
UBANGIJI ya ƙi su biyu.

16 Mene ne amfanin kuɗi a hannun wawa,
da yake ba shi da sha'awar samun hikima?

17 Aboki yakan yi ƙauna a koyaushe,
ɗan'uwa kuma, ai, don ɗaukar nawayar juna ne aka haife shi.

18 Mutumin da ba shi da azanci yakan ɗauki lamunin wani
ya kuma ɗauki nauyin biyan basusuwan maƙwabci.

19 Duk mai son faɗa yana son zunubi,
duk wanda ya gina ƙofar shiga mai tsawo yana gayyatar hallaka.

20 Mutum mai muguwar zuciya ba ya cin gaba;
duk wanda yake da harshen ruɗu kan shiga wahala.

21 Kasance da wawa kamar ɗa yakan kawo baƙin ciki
babu farin ciki ga mahaifin wawa.

22 Zuciya mai farin ciki magani ne mai kyau,
amma bakin rai kan busar da ƙasusuwa.

23 Mugun mutum yakan karɓa cin hanci a asirce
don yǎ lalace yin adalci.

24 Mutum mai basira kan kafa idonsa a kan hikima,
amma idanun wawa suna a kan ƙarshen duniya.

25 Da yake wawa yakan kawo baƙin ciki ga mahaifinsa
da ɓacin rai ga wanda ya haife shi.

26 Ba shi da kyau a hukunta marar laifi,
ko a bulale shugaba saboda mutuncinsu.

27 Mutum mai sani yakan yi la'akari da amfani da kalmomi,
mutum mai basira kuma natsattse ne.

28 Ko wawa in bai buɗe bakinsa ba, za a zaci shi mai hikima ne,
da kuma mai basira inda ya ƙame bakinsa.

## 18

1 Mutumin da ba ya abokantaka yakan nema ya cika burinsa ne kaɗai;
yakan ƙi yarda da kowace maganar da take daidai.

2 Wawa ba ya sha'awa ya sami fahimta
amma abin da yake so ya yi kaɗai, shi ne ya ba da ra'ayinsa.

3 Sa'ad da mugunci ya zo, reni ma kan zo,
haka kuma sa'ad da kunya ta zo, shan kunya kan biyo.

4 Kalmomin bakin mutum suna da zurfi kamar ruwaye,
amma maɓulɓulan hikima rafi ne mai gudu.

5 Ba shi da kyau ka yi wa mugu alheri
ko ka hana wa marar laifi adalci.

6 Leɓunan wawa kan jawo masa faɗa,
bakinsa kuma kan gayyaci dūka.

7 Bakin wawa lalatar da kansa yake yi
leɓunansa kuma tarko ne ga ransa.

8 Kalmomin mai gulma kamar abinci mai daɗi suke;
sukan gangara zuwa can cikin gaɓoɓin mutum.

9 Wanda yake ragwanci a aikinsa
ɗan'uwa ne ga wanda yakan lalatar da abubuwa.

10 Sunan Ubangiji hasumiya ce mai ƙarfi;
masu adalci kan gudu zuwa wurinta don su zauna lafiya.

11 Dukiyar masu arziki ita ce birninsu mai katanga;
suna gani cewa ba za a iya huda katangar ba.

12 Kafin fāɗuwarsa zuciyar mutum takan yi girman kai,
amma sauƙinkai kan zo kafin girmamawa.

13 Duk wanda yakan ba da amsa kafin ya saurara,
wannan wauta ce da kuma abin kunya.

14 Sa rai da mutum ke yi kan taimake shi sa'ad da yake ciwo,
amma in ya karai, to, tasa ta ƙare.

15 Zuciya mai la'akari kan nemi sani;
kunnuwan mai hikima kan bincika don yă koya.

16 Kyauta kan buɗe hanya wa mai bayarwa
yakan kuma kai shi a gaban babban mutum.

17 Wanda ya fara mai da jawabi yakan zama kamar shi ne mai gaskiya,
sai wani ya fito ya yi masa tambaya tukuna.

18 Jefa ƙuri'a kan daidaita tsakanin masu faɗa
ta kuma ajiye masu faɗan a rabe.

19 Ɗan'uwan da aka yi wa laifi ya fi birni mai katanga wuyan shiryawa,
kuma faɗace-faɗace suna kama da ƙofofin ƙarfe na fada.

20 Daga abin da baki ya furta ne cikin mutum kan cika;
girbi daga leɓunansa kuma yakan ƙoshi.

21 Harshe yana da ikon rai da mutuwa,
kuma waɗanda suke ƙaunarsa za su ci amfaninsa.

22 Duk wanda ya sami mace ya sami abu mai kyau
ya kuma sami tagomashi daga UBANGIJI.

23 Matalauci kan yi roƙo da taushi,
amma mawadaci kan amsa da kakkausar murya.

24 Mutum mai abokai masu yawa kan lalace,
amma akwai abokin da yakan manne kurkusa fiye da ɗan'uwa.

## 19

1 Gara matalauci wanda yake marar laifi
da wawa wanda leɓunansa masu ƙarya ne.

2 Ba shi da kyau ka kasance da niyya babu sani,
ko ka kasance mai garaje ka ɓace hanya.

3 Wautar mutum kan lalatar da ransa,
duk da haka zuciyarsa kan ba wa UBANGIJI laifi.

4 Wadata kan kawo abokai da yawa,
amma abokin matalauci kan bar shi.

5 Mai ba da shaidar ƙarya ba zai tafi babu hukunci ba,
kuma duk wanda ya baza ƙarairayi ba zai kuɓuta ba.

6 Kowa na ƙoƙari ya sami farin jini wurin mai mulki,
kuma kowa na so a ce shi abokin mutumin nan mai yawan kyauta ne.

7 'Yan'uwan matalauci sukan guje shi,
balle abokansa, su ma za su guje shi.
Ko da yake matalaucin yana binsu yana roƙo,
ba zai sam su ba.

8 Duk wanda ya sami hikima yana ƙaunar ransa;
duka wanda yake jin daɗi fahimi kan ci gaba.

9 Mai shaidar ƙarya ba zai tafi babu hukunci ba,
kuma duk mai baza ƙarairayi zai hallaka.

10 Bai dace da wawa ya yi rayuwa cikin jin daɗi ba,
haka ya fi muni bawa ya yi mulki a kan sarki!

11 Hikimar mutum kan ba shi haƙuri;
ɗaukakarsa ce ya ƙyale laifi.

12 Fushin sarki yana kama da rurin zaki,
amma tagomashinsa yana kama da raba a kan ciyawa.

13 Wawan yaro lalacin mahaifinsa ne,
mace mai yawan faɗa tana kama da ɗiɗɗigar ruwa.

14 Ana gādon dawakai da wadata daga iyaye ne,
amma mace mai basira daga UBANGIJI ne.

15 Ragwanci kan jawo zurfin barci,
mutum mai sanyin jiki kuma yana tare da yunwa.

16 Duk wanda ya bi umarnai kan tsare ransa,
amma duk wanda ya ƙi binsu zai mutu.

17 Duk wanda yake kirki ga matalauta yana ba wa UBANGIJI bashi ne,
zai kuwa sami lada game da abin da ya yi.

18 Ka hori ɗanka, gama yin haka akwai sa zuciya;
kada ka goyi baya lalacewarsa.

19 Dole mai zafin rai yă biya tara;
in ka fisshe shi sau ɗaya, to, sai ka sāke yin haka.

20 Ka kasa kunne ga shawara ka kuma yarda da umarni,
a ƙarshe kuwa za ka yi hikima.

21 Da yawa ne shirye-shiryen zuciyar mutum,
amma manufar UBANGIJI ce takan cika.

22 Abin da mutum yake sha'awa shi ne ƙauna marar ƙarewa;*
gara ka zama matalauci da ka zama maƙaryaci.

23 Tsoron UBANGIJI yakan kai ga rai.
Sa'an nan mutum ya sami biyan bukata, ba abin da zai cuce shi.

24 Rago kan sa hannunsa a kwano
ba ya ma iya ɗaga shi ya kai bakinsa!

25 Ka bulale mai ba'a, marasa azanci kuwa za su yi la'akari;
ka tsawata wa mai basira, zai kuwa ƙara sani.

26 Duk wanda ya yi wa mahaifinsa fashi ya kuma kori mahaifiyarsa
ɗa ne da kan kawo kunya da wulaƙanci.

27 In ka daina jin umarni, ɗana,
za ka kuwa kauce daga kalmomin sani.

28 Mai shaidar da yake malalaci yana wa shari'a ba'a ne,
bakin mugaye kuma na haɗiye mugunta.

29 An shirya tara saboda masu ba'a ne,

* **19:22** Ko kuwa Haɗamar mutum ita ce rashin kunyarsa

dūka kuma saboda bayan wawaye.

# 20

1 Ruwan inabi mai yin ba'a ne, barasa kuma mai rikici ne;
duk wanda suka sa ya kauce marar hikima ne.

2 Fushin sarki yana kama da rurin zaki;
duk wanda ya sa shi fushi zai rasa ransa.

3 Bangirma ne ga mutum ya guji faɗa,
amma kowane wawa yana saurin yin faɗa.

4 Rago ba ya noma a lokacin noma;
saboda haka a lokacin girbi ba ya bukata samun kome.

5 Manufofin zuciyar mutum zurfafan ruwaye ne,
amma mutum mai basira yakan jawo su.

6 Kowane mutum gani yake shi mai ƙauna marar ƙarewa ne,
amma ina? Da ƙyar ka sami amintacce mutum guda.

7 Mai adalci kan yi rayuwa marar abin zargi;
masu albarka ne 'ya'yan da za su biyo bayansa.

8 Sa'ad da sarki ya zauna kan kujerarsa don yă yi shari'a,
yakan ga dukan mugunta da idanunsa.

9 Wa zai iya cewa, "Na kiyaye zuciyata da tsarki;
ni mai tsabta ne marar zunubi kuma"?

10 Ma'auni marar gaskiya da magwajin da ba daidai ba,
UBANGIJI ya ƙi su duka.

11 Akan san ƙananan yara ta ayyukansu,
ana iya sani ko rayuwarsu amintattu ne, mai nagarta.

12 Kunnuwan da suke ji da kuma idanun da suke gani,
UBANGIJI ne ya yi su duka.

13 Kada ka so barci in ba haka ba za ka talauce;
ka zauna a faɗake za ka kuwa kasance da sauran abinci.

14 "Kai, ya yi tsada, ya yi tsada!" In ji mai saya;
sa'ad da ya tafi yana taƙama a kan ya iya ciniki.

15 Zinariya akwai ta, lu'ulu'u kuma ga shi a yalwace,
amma leɓunan da suke magana da sani suna da wuyan samu kamar duwatsu masu daraja.

16 A karɓi rigunan wanda ya ɗauki lamunin baƙo;

a riƙe shi jingina in ya yi shi don mace marar aminci.

17 Abincin da aka samu ta hanyar zamba yakan zama da daɗi,
amma mutum zai ƙarasa da baki cike da yashi.

18 Ka yi shirye-shirye ta wurin neman shawara;
in kana yaƙi, ka sami bishewa.

19 Mai gulma yakan lalace yarda;
saboda haka ka guji mutum mai yawan surutu.

20 In mutum ya zargi mahaifinsa ko mahaifiyarsa,
fitilarsa za tă mutu a tsakiyar duhu.

21 Gādon da aka samu da sauri a farkon farawa
ba zai zama mai albarka a ƙarshe ba.

22 Kada ka ce, "Zan rama wannan abin da aka yi mini!"
Ka dogara ga UBANGIJI, zai kuwa fisshe ka.

23 UBANGIJI ya ƙi ma'aunin da ba daidai ba,
da kuma magwajin da ba su gamshe shi ba.

24 UBANGIJI ne yake bi da matakan mutum,
Ta yaya wani zai fahimci hanyarsa?

25 Tarko ne ga mutum ya keɓe wani abu da ba tunani
daga baya kuma ya yi la'akari da alkawarinsa.

26 Sarki mai hikima yakan gane mugunta;
ya hukunta su ba tausayi.

27 Fitilar UBANGIJI kan bincika zuciyar mutum
takan bincika lamirinsa.

28 Kauna da aminci kan kiyaye sarki lafiya;
ta wurin ƙauna sarautarsa za tă zauna a kafe.

29 Ɗaukakar matasa maza ita ce ƙarfinsu,
furfura ita ce darajar tsofaffi.

30 Naushi da rauni kan share mugunta,
dūka kuma kan tsabtacce lamiri.

# 21

1 A hannun UBANGIJI zuciyar sarki kamar ruwan rafi ne
wanda yake bi da shi duk inda ya so.

2 Mutum zai yi tunani hanyoyinsa daidai suke,
amma UBANGIJI yakan auna zuciya.

3 Yin abin da yake daidai da kuma nagari
Ubangiji ya fi yarda da shi fiye da hadaya.

4 Girmankai da fariya,
su ne fitilar mugaye, wannan kuwa zunubi ne!

5 Shirye-shiryen mai aiki tuƙuru kan kai ga riba
in kuwa ka cika gaggawa zai kai ga talauci.

6 Dukiyar da aka samu ta wurin harshe mai yin ƙarya
tarin tururi ne da kuma mugun tarko.

7 Rikicin mugaye zai yi gāba da su,
gama sun ƙi su yi abin da yake daidai.

8 Hanyar mai laifi karkatacciya ce,
amma halin marar laifi sukan aikata gaskiya.

9 Gara a zauna a kusurwar rufin ɗaki
da a zauna a gida ɗaya da mace mai fitina.

10 Mugun mutum yakan zaƙu ya aikata mugunta;
maƙwabcinsa ba ya samun jinƙai daga gare shi.

11 Sa'ad da aka hukunta mai ba'a marasa azanci suka yi wayo;
sa'ad da aka yi wa mai hikima umarni yakan sami sani.

12 Mai Adalci kan lura da gidan mugu
kan kuma zama sanadin lalacin mugu.

13 In mutum ya toshe kunnuwansa ga kukan matalauci,
shi ma zai yi kukan neman taimako ba kuwa zai sami amsa ba.

14 Kyautar da aka yi a asirce takan kwantar da fushi,
kuma cin hancin da aka rufe a cikin riga kan tā da fushi mai tsanani.

15 Sa'ad da aka yi adalci, yakan kawo farin ciki ga mai adalci
amma fargaba ga masu aikata mugunta.

16 Mutumin da ya kauce daga hanyar fahimi
kan zo ga hutu a ƙungiyar matattu.

17 Duk mai son jin daɗi zai zama matalauci;
duk mai son ruwan inabi da mai ba zai taɓa zama mai arziki ba.

18 Mugu kan zama abin fansa don adali,
marar aminci kuma don mai aikata gaskiya.

19 Gara a zauna a hamada
da a zauna da mace mai fitina da kuma mugun hali.

20 A gidan mai hikima akwai wuraren ajiya na abinci da mai masu kyau,
amma wawa kan cinye duk abin da yake da shi.

21 Duk wanda ya nemi adalci da ƙauna
kan sami rai, wadata da girmamawa.

22 Mutum mai hikima kan fāɗa wa birnin jarumawa
ya kuma rushe katangar da suka dogara a kai.

23 Duk wanda yake lura da bakinsa da kuma harshensa
kan kiyaye kansa daga masifa.

24 Mai girmankai da kuma mai fariya, "Mai ba'a" ne sunansa;
yana yin abubuwa da girmankai ainun.

25 Marmarin rago zai zama mutuwarsa,
domin hannuwansa sun ƙi su yi aiki.
26 Dukan yini yana marmari ya sami ƙari,
amma mai adalci yakan bayar hannu sake.

27 Hadayar mugaye abin ƙyama ne,
balle ma in aka kawo da mugun nufi!

28 Mai ba da shaidar ƙarya zai hallaka,
kuma duk wanda ya saurare shi zai hallaka har abada.*

29 Mugun mutum kan yi tsayin daka,
amma mai aikata gaskiya kan yi tunani a kan abin da yake yi.

30 Babu hikima, babu tunani, babu shirin
da zai yi nasara a kan UBANGIJI.

31 Akan shirya doki domin ranar yaƙi,
amma nasara tana ga UBANGIJI ne.

# 22

1 An fi son suna mai kyau fiye da wadata mai yawa;
tagomashi kuma ya fi azurfa ko zinariya.

2 Mawadaci da matalauci suna da abu guda.
UBANGIJI ne Mahaliccinsu duka.

3 Mai basira kan ga damuwa tana zuwa yă nemi mafaka,
amma marar azanci kan yi ta tafiya yă kuma sha wahala.

4 Sauƙinkai da tsoron UBANGIJI
sukan kawo wadata da girmamawa da kuma rai.

---

* **21:28** Ko kuwa / amma kalmomin mai biyayya za su ci gaba da kasancewa

5 A hanyoyin mugu akwai kaya da tarko,
amma duk wanda ya kiyaye ransa kan kauce musu.

6 Ka hori yaro a hanyar da ya kamata yă bi,
kuma sa'ad da ya tsufa ba zai bar ta ba.

7 Mawadaci yakan yi mulki a kan matalauci,
mai cin bashi kuwa bawan mai ba da bashi ne.

8 Duk wanda ya shuka mugunta yakan girbe wahala,
za a kuma hallaka sandar fushinsa.

9 Mai bayarwa hannu sake shi kansa zai sami albarka,
gama yakan raba abincinsa da matalauta.

10 Ka hori mai ba'a, hatsaniya kuwa za tă yi waje;
fitina da zargi kuma za su ƙare.

11 Duk mai son tsabtar zuciya wanda kuma jawabinsa mai alheri ne
zai zama aminin sarki.

12 Idanun UBANGIJI na lura da sani,
amma yakan ƙi kalmomin marar aminci.

13 Rago kan ce, "Akwai zaki a waje!"
Ko kuma "Za a kashe ni a tituna!"

14 Bakin mazinaciya rami ne mai zurfi;
duk wanda yake a ƙarƙashin fushin UBANGIJI zai fāɗa a ciki.

15 Wauta tana da yawa a zuciyar yara,
amma sandar horo zai kore ta nesa da su.

16 Duk wanda yake danne matalauta don yă azurta
kuma duk wanda yake kyauta ga mawadata, dukansu kan talauta.

## Maganganu Masu Hikima

*Faɗi 1*

17 Ka kasa kunne ka kuma saurara ga maganganu masu hikima;
ka yi amfani da abin da nake koyarwa,
18 gama yana da daɗi sa'ad da ka kiyaye su a zuciyarka
ka kuma kasance da su a shirye a leɓunanka.
19 Domin dogarawarka ta kasance ga UBANGIJI,
ina koya maka yau, har kai ma.
20 Ban rubuta maka maganganu talatin ba,
maganganun shawara da sani,
21 ina koya maka gaskiya da kalmomin da za ka dogara a kai,
saboda ka iya ba da amsa daidai
ga duk wanda ya aike ka?

*Faɗi 2*

22 Kada ka zalunci matalauta a kan suna matalauta
kada kuma ka ƙwari wanda ba shi da mai taimako a gaban shari'a,

23 gama UBANGIJI zai yi magana dominsu
zai kuwa washe waɗanda suka washe su.

*Faɗi 3*
24 Kada ka yi abokantaka da mai zafin rai,
kada ka haɗa kai da wanda ba shi da wuya ya yi fushi,
25 in ba haka ba za ka koyi hanyoyinsa
ka kuma sa kanka a tarko.

*Faɗi 4*
26 Kada ka zama mai ɗaukar lamuni
ko ka ba da jingina saboda bashi;
27 gama in ka kāsa biya
za a ƙwace gadon da kake kwanciya a kai ma.

*Faɗi 5*
28 Kada ka matsar da shaidar kan iyakar
da kakanninka suka kafa.

*Faɗi 6*
29 Kana ganin mutumin da yake da gwaninta a cikin aikinsa?
Zai yi wa sarakuna hidima;
ba zai yi hidima wa mutanen da ba su iya ba.

## 23

*Faɗi 7*
1 Sa'ad da ka zauna domin cin abinci da mai mulki,
ka lura sosai da abin da yake gabanka,
2 ka kuma sa wuƙa a maƙogwaronka
in kai mai ci da yawa ne.
3 Kada ka yi marmarin abincinsa mai daɗi
gama wannan abinci ruɗu ne.

*Faɗi 8*
4 Kada ka gajiyar da kanka don ka yi arziki;
ka kasance da hikimar dainawa.
5 Da ƙyiftawar ido a kan wadata ta ɓace,
gama tabbatacce sukan yi fikafikai
sukan tashi sama kamar gaggafa.

*Faɗi 9*
6 Kada ka ci abincin mai rowa,
kada ka yi marmarin abincinsa mai daɗi;
7 gama shi wani irin mutum ne
wanda kullum yana tunani game da tsadar abincin.*
Zai ce maka, "Ci ka sha,"
amma zuciyarsa ba ta tare da kai.
8 Za ka yi amai ɗan abin da ka ci
dukan daɗin bakinka kuwa zai tafi a banza.

*Faɗi 10*
9 Kada ka yi magana da wawa,
gama zai yi wa maganar hikimarka ba'a.

*Faɗi 11*

* **23:7** Ko kuwa gama yadda yake tunani a cikinsa, haka yake; Ko kuwa gama yadda ya sa a bikin, haka yake

10 Kada ka kawar da shaidar iyaka ta dā
ko ka ɗiba gonar marayu,
11 gama mai Kāriyarsu yana da ƙarfi;
zai kuwa yi magana dominsu.

*Faɗi 12*
12 Ka mai da hankali ga umarni
ka kuma kasa kunne ga kalmomin sani.

*Faɗi 13*
13 Kada ka bar yaro ba horo;
in ka yi masa horo da sanda, ba zai mutu ba.
14 Ka hukunta shi da sanda
ka ceci ransa daga mutuwa.

*Faɗi 14*
15 Ɗana, in zuciyarka mai hikima ce,
to, zuciyata za tă yi murna;
16 cikin cikina zai yi farin ciki
in leɓunanka suna maganar abin da yake daidai.

*Faɗi 15*
17 Kada ka bar zuciyarka tă yi ƙyashin masu zunubi,
amma kullum tsoron UBANGIJI za ka yi kishi.
18 Tabbatacce akwai sa zuciya ta nan gaba dominka,
kuma sa zuciyarka ba za tă zama a banza ba.

*Faɗi 16*
19 Ka saurara, ɗana, ka zama mai hikima,
ka kafa zuciyarka a hanyar da take daidai.
20 Kada ka haɗa kai da waɗanda suke shan ruwan inabi da yawa
ko masu haɗama kansu da abinci,
21 gama bugaggu da ruwan inabi da masu yawan ci sukan zama matalauta,
gama jiri yakan yi musu sutura da tsummoki.

*Faɗi 17*
22 Ka kasa kunne ga mahaifinka, wanda ya ba ka rai,
kada kuwa ka rena mahaifiyarka saʼad da ta tsufa.
23 Ka saye gaskiya kada kuwa ka sayar da ita;
ka nemi hikima, horo da fahimi.
24 Mahaifin adali yana da farin ciki sosai;
duk wanda yake da ɗa mai hikima yakan ji daɗinsa.
25 Bari mahaifinka da mahaifiyarka su yi murna;
bari wadda ta haife ka tă yi farin ciki!

*Faɗi 18*
26 Ɗana, ka ba ni zuciyarka
bari kuma idanunka su kiyaye hanyoyina,
27 gama karuwa rami ne mai zurfi
mace marar aminci matsattsiyar rijiya ce.
28 Kamar ʼyan fashi, takan kwanta tana jira
tana kuma ninka rashin aminci a cikin maza.

*Faɗi 19*
29 Wa yake wayyo? Wa yake baƙin ciki?
Wa yake neman fada? Wa yake gunaguni?

Wa yake da raunuka ba dalili? Wa yake da jan idanu?
30 Waɗanda suke daɗe suna shan ruwan inabi,
waɗanda suke neman ƙoƙon damammen ruwan inabi.
31 Kada ka ƙyifce ido a ruwan inabi sa'ad da ya yi ja,
sa'ad da yana da kyan gani a cikin ƙwarya,
sa'ad da yana gangarawa sumul a maƙogwaro!
32 A ƙarshe yana sara kamar maciji
da kuma dafi kamar gamsheƙa.
33 Idanunka za su riƙa gane-gane,
zuciyarka kuma za su riƙa tunani abubuwa masu rikitarwa.
34 Za ka zama kamar wanda yake barci a tsakiyar tekuna,
kwance a sama itacen jirgin ruwa.
35 Za ka ce "Sun buge ni, amma ban ji ciwo ba!
Sun daddoke ni, amma ba na jin zafinsa!
Yaushe zan farka
don in ƙara shan wani?"

# 24

*Faɗi 20*

1 Kada ka yi ƙyashin mugaye,
kada ka yi sha'awar ƙungiyarsu;
2 gama leɓunansu suna maganar tā-da-na-zaune-tsaye ne.

*Faɗi 21*

3 Ta wurin hikima ce ake gina gida,
kuma ta wurin fahimi ake kafa ta;
4 ta wurin sani ɗakunanta sukan cika
da kyawawan kayayyaki masu daraja.

*Faɗi 22*

5 Mutum mai hikima yana da iko sosai,
kuma mutum mai sani yakan ƙaru da ƙarfi;
6 don yin yaƙi kana bukatar bishewa,
kuma don ka yi nasara kana bukatar mashawarta masu yawa.

*Faɗi 23*

7 Hikima ta yi wa wawa nisa ƙwarai
a cikin taro a ƙofar gari ba shi da ta cewa.

*Faɗi 24*

8 Duk mai ƙulla mugunta
za a ɗauka shi mai kuta hargitsi ne.
9 Makircin wawa zunubi ne,
mutane kuma sukan yi ƙyamar mai ba'a.

*Faɗi 25*

10 In ba ka da ƙarfi a lokacin wahala,
ka tabbatar kai marar ƙarfi ne sosai!
11 Ka kuɓutar da waɗanda ake ja zuwa inda za a kashe su;
ka riƙe waɗanda suke tangaɗi zuwa wajen yanka.
12 In kuka ce, "Ai, ba mu san wani abu a kai wannan ba,"
shi da yake awon ba shi da zuciyar ganewa ne?
Shi da yake tsare ranka bai sani ba ne?
Ba zai sāka wa kowane mutum bisa ga abin da ya aikata ba?

*Faɗi 26*
13 Ka sha zuma, ɗana, ka sha zuma gama tana da kyau;
zuma daga kaki yana da zaƙi a harshenka.
14 Ka kuma san cewa hikima tana da zaƙi ga rai;
in ka same ta, akwai sa zuciya ta nan gaba dominka,
kuma sa zuciyarka ba za tă zama a banza ba.

*Faɗi 27*
15 Kada ka kwanta kana fako kamar ɗan iska don ƙwace gidan adali,
kada ka ƙwace masa wurin zama;
16 gama ko da adali ya fāɗi sau bakwai, yakan tashi kuma,
amma bala'i kan kwantar da mugaye.

*Faɗi 28*
17 Kada ka yi dariya sa'ad da abokin gāba ya fāɗi;
sa'ad da ya yi tuntuɓe, kada ka yi farin ciki,
18 in ba haka ba in UBANGIJI ya gani ba zai amince ba
ya kuma juye fushinsa daga gare shi.

*Faɗi 29*
19 Kada ka ji tsoro saboda masu mugunta
ko ka yi ƙyashin mugaye,
20 gama mugu ba shi da zuciya ta nan gaba,
kuma fitilar mugaye za tă mutu.

*Faɗi 30*
21 Ka ji tsoron UBANGIJI da kuma sarki, ɗana,
kuma kada ka haɗa kai da masu tayarwa,
22 gama za a tura waɗannan biyu zuwa hallaka nan da nan,
kuma wa ya sani irin bala'in da za su iya kawowa?

## Karin maganganun hikima

23 Waɗannan ma maganganun masu hikima ne,
Nunan sonkai a shari'a ba shi da kyau.
24 Duk wanda ya ce wa mai laifi, "Ba ka da laifi",
mutane za su la'ance shi al'umma kuma za tă ce ba a san shi ba.
25 Amma zai zama da lafiya ga duk waɗanda suka hukunta masu laifi,
kuma babban albarka zai zo a kansu.

26 Amsa da take ta gaskiya
tana kamar sumba a leɓuna.

27 Ka gama aikinka
ka kuma shirya gonakinka;
bayan haka, ka gina gidanka.

28 Kada ka ba da shaida a kan maƙwabcinka ba tare da isashen dalili ba,
ko ka yi amfani da leɓunanka ka yi ruɗu.
29 Kada ka ce, "Zan yi masa kamar yadda ya yi mini;
zan rama abin da wannan mutum ya yi mini."

30 Na wuce cikin gonar rago,
na wuce cikin gonar inabin mutumin da ba shi da azanci;
31 ƙayayyuwa sun yi girma ko'ina,
ciyayi sun rufe ƙasar,

katangar duwatsu duk ta rushe.
32 Na yi tunani a zuciyata
na kuwa koyi darasi daga abin da na gani.
33 Ɗan barci, ɗan gyangyaɗi,
ɗan naɗin hannuwa don a huta,
34 sai talauci ya shigo maka kamar ʼyan fashi
rashi kuma ya zo maka kamar mai hari.

## Karin karin maganar Solomon

# 25

1 Waɗannan ƙarin karin maganar Solomon ne waɗanda mutanen Hezekiya sarkin
Yahuda suka tara.
2 Ɗaukakar Allah ce a ɓoye batun;
a bayyana batun kuwa ɗaukakar sarakuna ne.
3 Kamar yadda sammai suna can bisa duniya kuma tana da zurfi,
haka zukatan sarakuna suka wuce a bincika.

4 Ka tace azurfa
sai kayan su fito don maƙerin azurfa;
5 ka cire mugaye daga gaban sarki,
kursiyinsa kuwa zai kahu ta wurin adalci.

6 Kada ka ɗaukaka kanka a gaban sarki,
kada kuma ka nemi wa kanka wuri a cikin manyan mutane;
7 gara ya ce maka, "Ka hauro nan,"
da a ƙasƙantar da kai a gaban wani mai makami.

Abin da ka gani da idanunka
8 kada ka yi garaje kai ƙara a majalisa,
gama me za ka yi a ƙarshe
in maƙwabcinka ya ba ka kunya?

9 In kai da maƙwabcinka kuka yi gardama,
kada ka tona asirin wani,
10 in ba haka ba duk wanda ya ji zai kunyata ka
ba za ka kuma taɓa rabuwa da wannan mummuna suna ba.

11 Kalmar da aka faɗa daidai
tana kamar zubin zinariyar da aka yi a mazubin azurfa.
12 Kamar ʼyan kunnen zinariya ko kuwa kayan ado na zinariya zalla
haka yake da tsawatawar mai hikima ga kunne mai saurarawa.

13 Kamar sanyin ƙanƙara a lokacin girbi
haka ɗan saƙo mai aminci wanda aka aika;
ya wartsakar da ran waɗanda suka aike shi.
14 Kamar gizagizai da kuma iska marar ruwan sama
haka mutumin da yake fariya a kan kyautan da ba ya bayarwa.

15 Ta wurin haƙuri akan rinjaye mai mulki,
magana mai hankali kan karye ƙashi.

16 In ka sami zuma, ka sha isashe kawai,
in ya yi yawa, za ka yi amai.
17 Kada ka cika ziyarar gidan maƙwabcinka
yawan ganinka zai sa ya ƙi ka.

18 Kamar sanda ko takobi ko kibiya mai tsini
haka yake da mutumin da yake ba da shaidar ƙarya a kan maƙwabcinsa.
19 Kamar haƙori mai ciwo ko yin tafiya da gurguwar ƙafa
haka yake ga mai dogara da marasa aminci a lokacin wahala.
20 Kamar wanda ya tuɓe riga a ranar da ake sanyi,
ko kuwa kamar zuba ruwan tsami a kanwa,
haka yake da mai rera waƙoƙi ga mai baƙin ciki.

21 In abokin gābanka yana jin yunwa, ka ba shi abinci ya ci;
in yana jin ƙishi, ka ba shi ruwa ya sha.
22 Ta yin haka, za ka tara garwashin wuta mai ci a kansa,
UBANGIJI kuma zai sāka maka.

23 Kamar yadda iskar arewa kan kawo ruwan sama,
haka jita-jita kan kawo fushi.

24 Gara a zauna a kusurwar rufin ɗaki
da a zauna a gida ɗaya da mace mai fitina.

25 Kamar ruwan sanyi ga ran da ya gaji
haka yake da jin labari mai daɗi daga ƙasa mai nisa.
26 Kamar rafi mai laka ko rijiyar da ta gurɓace
haka yake da mai adalci wanda ya miƙa wuya ga mugaye.

27 Ba shi da kyau ka sha zuma da yawa,
haka ma ba shi da kyau ka nemi girma wa kanka.

28 Kamar birni da katangarsa sun rushe
haka yake da mutumin da ba ya iya danne fushinsa.

## 26

1 Kamar ƙanƙara a rani ko ruwan sama a lokacin girbi,
haka girmamawa bai dace da wawa ba.
2 Kamar gwara mai yawo ko alallaka mai firiya,
haka yake da la’anar da ba tă dace tă kama ka ba take.
3 Bulala don doki, linzami don jaki,
sanda kuma don bayan wawaye!
4 Kada ka amsa wa wawa bisa ga wautarsa,
in ba haka ba kai kanka za ka zama kamar sa.
5 Ka amsa wa wawa bisa ga wautarsa,
in ba haka ba zai ga kansa mai hikima ne.
6 Kamar datsewar ƙafafun wani ko shan dafi
haka yake da a aika da saƙo ta hannun wawa.
7 Kamar ƙafafun gurgun da suka yi laƙwas
haka karin magana yake a bakin wawa.
8 Kamar ɗaura dutse a majajjawa

haka yake da girmama wawa.
9 Kamar suƙar ƙaya a hannun wanda ya bugu
haka karin magana yake a bakin wawa.
10 Kamar maharbi wanda yake jin wa kowa rauni
haka yake da duk wanda ya yi hayan wawa ko wani mai wucewa.
11 Kamar yadda kare kan koma ga amansa,
haka wawa kan maimaita wautarsa.
12 Gwamma riƙaƙƙen wawa
da mutum mai ganin kansa mai hikima ne.

13 Rago yakan ce, "Akwai zaki a kan hanya,
zaki mai faɗa yana yawo a tituna!"
14 Kamar yadda ƙofa kan juya a ƙyaurensa,
haka rago yake jujjuya a gadonsa.
15 Rago kan sa hannunsa a kwano
ba ya ma iya ɗaga shi ya kai bakinsa.
16 Rago yana gani yana da hikima
fiye da mutane bakwai da suke ba da amsa da dalilai a kan ra'ayinsu.

17 Kamar wani da ya kama kare a kunnuwa
haka yake da mai wucewa da ya tsoma baki a faɗan da ba ruwansa.

18 Kamar yadda mahaukaci yake harbin
cukwimai ko kibiyoyi masu dafi
19 haka yake da mutumin da ya ruɗe maƙwabci
sa'an nan ya ce, "Wasa ne kawai nake yi!"

20 In ba itace wuta takan mutu;
haka kuma in ba mai gulma ba za a yi faɗa ba.
21 Kamar yadda gawayi yake ga murhu, itace kuma ga wuta,
haka mutum mai neman faɗa yake ga faɗa.
22 Kalmomin mai gulma suna kama da burodi mai daɗi;
sukan gangara can cikin cikin mutum.

23 Kamar kaskon da aka dalaye da azurfar da ba a tace ba
haka leɓuna masu mugun zuciya.
24 Mai yin ƙiyayya yakan ɓoye kansa da maganar bakinsa,
amma a cikin zuciyarsa yana cike da munafunci
25 Ko da jawabinsa ya ɗauki hankali, kada ka gaskata shi,
gama abubuwa ƙyama guda bakwai sun cika zuciyarsa.
26 Wataƙila ya ɓoye ƙiyayyarsa da ƙarya,
duk da haka za a tone muguntarsa a cikin taro.
27 In mutum ya haƙa rami, shi zai fāɗi a ciki;
in mutum ya mirgino dutse, dutsen zai mirgine a kansa.
28 Harshe mai faɗin ƙarya yana ƙin waɗanda yake ɓata musu rai,
daɗin baki kuma yakan aikata ɓarna.

## 27

1 Kada ka yi fariya a kan gobe
gama ba san abin da ranar za tă kawo ba.

2 Ka bar wani ya yabe ka, ba kai kanka ba;
wani dabam, ba leɓunanka ba.

3 Dutse yana da nauyi yashi kuma wahala ce,
amma tsokanar wawa ta fi su duka nauyi.

4 Fushi mugun abu ne mai hallakarwa,
amma wa zai iya tsaya a gaban kishi?

5 Gara tsawatawar da ake yi a fili
da ƙaunar da ake yi a ɓoye.

6 Za a iya amince da rauni daga aboki,
amma abokin gāba ko da ya sumbace ka kada ka sake da shi!

7 Duk wanda ya ƙoshi da zuma, ba ya marmarinsa kuma
amma wanda yake yunwa ko abin da yake da ɗaci ma zai ji shi da zaƙi.

8 Kamar tsuntsun da ya ɓace daga sheƙarsa
haka yake da mutumin da ya bar gidansa.

9 Man shafawa mai ƙanshi da kuma turare kan faranta zuciya,
gaisuwar amini kuma takan fito daga shawarar kirki.

10 Kada ka manta da abokinka da kuma abokin mahaifinka,
kuma kada ka tafi gidan ɗan'uwanka sa'ad da masifa ta same ka,
gara ka je wurin maƙwabci na kusa da ka je wurin ɗan'uwan da yake da nisa.

11 Ka zama mai hikima, ɗana, ka kuma faranta mini zuciya;
zan iya amsa kowace irin suƙar da wani zai yi mini.

12 Mai basira kan hango hatsari ya kuma kauce,
marar azanci zai yi ta kutsa kai ciki, daga baya ya yi da na sani.

13 A karɓe rigunan wanda ya ɗauki lamunin baƙo;
a riƙe shi jingina in ya yi shi don mace marar aminci.

14 In mutum ya albarkaci maƙwabcinsa da murya mai ƙarfi da sassafe,
za a ɗauka shi a matsayin la'ana.

15 Mace mai fitina kamar
ɗiɗɗigar ruwa take ba ƙaƙƙautawa;
16 hana ta yana kamar yin ƙoƙari tsai da iska ne
ko yin ƙoƙarin cafke mai a tafin hannunka.

17 Kamar yadda ƙarfe kan wasa ƙarfe
haka mutum kan koyi daga mutum.

18 Duk wanda ya lura da itacen ɓaure, zai ci 'ya'yansa,
kuma duk wanda ya lura da maigidansa za a girmama shi.

19 Kamar yadda ruwa kan nuna yadda fuska take,
haka zuciyar mutum kan nuna irin mutumin.

20 Mutuwa da Hallaka* ba sa ƙoshi,
haka idanun mutum ba sa ƙoshi da gani.

21 Ana gwajin azurfa da kuma zinariya da wuta,
amma akan gwada mutum ta wurin yabon da ya samu.

22 Ko da ka daka wawa a turmi,
kana daka shi kamar hatsi da taɓarya,
ba za ka fid da wauta daga gare shi ba.

23 Ka tabbata ka san lafiyar garken tumakinka,
ka mai da hankali ga garken shanunka;
24 domin dukiya ba ta dawwama har abada,
ba a kuma kasance da rawani daga tsara zuwa tsara.
25 Sa'ad da aka yanki ingirci sabon toho kuma ya bayyana
aka kuma tattara ciyawa daga tuddai,
26 gashin raguna za su tanada maka tufafi,
za ka iya sayi gonaki masu kyau da kuɗin awaki.
27 Za ka kasance da madarar awaki mai yawa
don ka ciyar da kanka da kuma iyalinka
ka kuma inganta bayinka mata.

# 28

1 Mugu yakan gudu ko babu wanda yake korarsa,
amma adalai suna da ƙarfin hali kamar zaki.

2 Sa'ad da ƙasa ta yi tayarwa, takan kasance da masu mulki da yawa,
amma mai fahimi da sani kan mai da zaman lafiya.

3 Mai mulkin da ya danne talakawa
yana kama da ruwan saman da ya lalatar da hatsi.

4 Duk waɗanda ba sa bin doka yabon mugaye suke yi,
amma waɗanda suke yin biyayya da doka suna gāba da mugaye ke nan.

5 Mugaye ba su san gaskiya ba,
amma waɗanda suke neman Ubangiji sun santa sosai.

6 Gara matalauci wanda yake tafiya babu abin zargi
da mai arziki wanda hanyoyinsa mugaye ne.

7 Duk wanda ya kiyaye doka ɗa ne mai la'akari,
amma wanda yake abokantaka da masu zari yakan jawo wa mahaifinsa kunya.

8 Duk wanda ya tara dukiyarsa ta wurin ba da bashi da ruwan da ya wuce misali
yana tara wa wani ne wanda zai yi wa talakawa alheri.

* 27:20 Da Ibraniyanci Sheol da Abaddon

9 In wani ya yi kunnuwa ƙashi ga doka
ko addu’arsa ma abar ƙyama ce.

10 Duk wanda ya jagorance masu aikata gaskiya a hanyar mugunta
zai fāɗa cikin tarkonsa
amma marasa abin zargi za su sami gādo mai kyau.

11 Mai arziki zai yi zato shi mai hikima ne a ganinsa,
amma matalauci mai basira ya fi shi sanin abin da yake daidai.

12 Sa’ad da adalai suka yi nasara, kowa yakan yi biki;
amma sa’ad da mugu ya samu shugabanci, mutane sukan yi ta ɓuya.

13 Duk wanda ya ɓoye zunubansa ba ya taɓa cin nasara,
amma duk wanda ya furta ya kuma ƙi su yakan sami jinƙai.

14 Mai albarka ne mutumin da kullum yake jin tsoron Allah,
amma duk wanda ya taurare zuciyarsa yakan shiga wahala.

15 Kamar rurin zaki ko sanɗar beyar
haka mugun mutum mai mulki a kan mutane marasa ƙarfi yake.

16 Mugu mai mulki ba shi da azanci,
amma duk wanda yake ƙin ƙazamar riba yakan yi tsawon rai.

17 Mutumin da laifin kisa ya yi ta damunsa
zai zama mai gudu don tsoro har mutuwa;
kada wani ya taimake shi.

18 Duk wanda ya yi tafiya marar abin zargi zai zauna lafiya,
amma duk wanda hanyoyinsa mugaye ne zai fāɗi nan da nan.

19 Duk wanda ya nome gonarsa zai sami amfani a yalwace,
amma duk wanda yake zaman banza zai zama matalauci a koyaushe.

20 Mutum mai aminci zai cika da albarka,
amma duk mai son yin arziki dare ɗaya zai sha hukunci.

21 Nuna sonkai ba shi da kyau,
duk da haka mutum zai aikata abin da ba daidai ba saboda ’yar ƙaramar rashawa.

22 Mai rowa yana alla-alla ya yi arziki
bai san cewa talauci ne ke jiransa ba.

23 Duk wanda ya tsawata wa wani mutum zai sami yabo a ƙarshe
fiye da wanda yake mai daɗin baki.

24 Duk wanda ya yi wa mahaifin ko mahaifiyarsa sata
ya kuma ce, “Ai, ba laifi ba ne”
abokin mai hallakarwa ne shi.

25 Mai haɗama yakan jawo tā-da-na-zaune-tsaye,
amma duk wanda ya dogara ga UBANGIJI zai yi nasara.

26 Duk mai dogara ga kansa wawa ne,
amma duk wanda yake tafiya da hikima zai zauna lafiya.

27 Duk wanda yake bayarwa ga matalauta ba zai rasa kome ba,
amma duk wanda bai kula da su ba yana samu la'ana masu yawa.

28 Sa'ad da mugu ya samu shugabanci, mutane sukan yi ta ɓuya;
amma sa'ad da mugu ya hallaka, adali kan ci gaba cikin arziki da lafiya.

# 29

1 Mutumin da ya ci gaba da taurinkai bayan an kwaɓe shi
ba da daɗewa ba zai hallaka ba makawa.

2 Sa'ad da masu adalci suke cin nasara, mutane kan yi farin ciki
sa'ad da mugaye suke mulki, mutane kan yi nishi.

3 Duk mai ƙaunar hikima kan kawo wa mahaifinsa farin ciki,
amma wanda yake ma'amala da karuwai kan lalatar da dukiyarsa.

4 Ta wurin yin adalci sarki kan sa ƙasa tă yi ƙarƙo
amma duk mai haɗama don cin hanci kan rushe ƙasar.

5 Duk wanda yake wa maƙwabcinsa daɗin baki
yana sa wa ƙafafunsa tarko ne.

6 Mugun mutum tarko ne ta wurin zunubinsa,
amma mai adalci zai iya rera ya kuma yi murna.

7 Masu adalci sun damu game da adalci don talakawa,
amma mugaye ba su da wannan damuwa.

8 Masu ba'a kan kuta faɗa a birni,
amma masu hikima sukan kwantar da fushi.

9 In mai hikima ya je wurin shari'a da wawa,
wawa kan yi ta fushi yana ta dariya, ba kuwa za a sami salama ba.

10 Masu kisankai sukan ƙi mutum mai mutunci
su kuma nema su kashe mai aikata gaskiya.

11 Wawa yakan nuna fushinsa a fili,
amma mai hikima kan kanne fushinsa.

12 In mai mulki yana sauraran ƙarairayi,
dukan ma'aikatansa za su zama mugaye.

13 Matalauci da azzalumi suna da wannan abu ɗaya.
UBANGIJI ne yake ba dukansu gani.

14 In sarki yana hukunta talakawa da adalci
kursiyinsa kullum zai kasance lafiya.

15 Sandar gyara kan ba da hikima,
amma yaron da aka bari ba horo kan jawo kunya ga mahaifiyarsa.

16 Sa'ad da mugaye suke cin nasara, haka zunubi zai yi ta ƙaruwa,
amma masu adalci za su ga fāɗuwar waɗannan mutane.

17 Ka hori ɗanka, zai kuwa ba ka salama;
zai ba ka farin cikin da kake so.

18 Inda ba wahayi, mutane kan kangare;
amma masu albarka ne waɗanda suke kiyaye doka.

19 Ba a yi wa bawa gyara ta wurin magana kawai;
ko da ya fahimta ma, ba zai kula ba.

20 Ka ga mutum mai yin magana da garaje?
To, gara a sa zuciya ga wawa da a sa zuciya gare shi.

21 In mutum ya yi wa bawansa shagwaɓa tun yana yaro,
zai jawo baƙin ciki a ƙarshe.

22 Mutum mai cika fushi yakan tā da faɗa,
mai zafin rai kuma kan yi zunubai masu yawa.

23 Fariyar mutum kan jawo masa ƙasƙanci
amma mai sauƙinkai kan sami girmamawa.

24 Duk wanda yake abokin ɓarawo abokin gāban kansa ne;
yana jin sa yana ta rantsuwa, amma bai isa ya ce kome ba.

25 Jin tsoron mutum tarko ne,
amma duk wanda ya dogara ga UBANGIJI zai zauna lafiya.

26 Mutane sukan nemi samun farin jini daga wurin sarki,
amma daga wurin UBANGIJI ne mutum kan sami adalci.

27 Masu adalci suna ƙyamar masu rashin gaskiya;
mugaye sukan yi ƙyamar masu aikata gaskiya.

## Maganganun Agur

# 30

1 Maganganun Agur ɗan Yake, magana ce horarriya.*
Wannan mutum ya furta wa Itiyel da kuma ga Ukal,

2 "Ni ne mafi jahilci a cikin mutane;
ba ni da fahimi irin na mutum.
3 Ban koyi hikima ba,

* **30:1** Ko kuwa Yake na Massa

ba ni kuma da sani game da Mai Tsarkin nan,
4 Wane ne ya taɓa haura zuwa sama ya dawo?
Wane ne ya tattara iska a tafin hannuwansa?
Wane ne ya nannaɗe ruwaye a cikin rigarsa?
Wane ne ya kafa dukan iyakokin duniya?
Mene ne sunansa, da kuma sunan ɗansa?
Faɗa mini in ka sani!

5 “Kowace maganar Allah ba ta da kuskure;
shi ne garkuwa ga waɗanda suke neman mafaka daga gare shi.
6 Kada ka ƙara ga maganarsa,
in ba haka ba zai tsawata maka ya kuma nuna kai maƙaryaci ne.

7 “Abu biyu ina roƙonka, ya Ubangiji;
kada ka hana ni kafin in mutu.
8 Ka kawar da ƙarya da kuma ƙarairayi nesa da ni;
kada ka ba ni talauci ko arziki,
amma ka ba ni abincina na yini kaɗai.
9 In ba haka ba, zan wadace in ƙi ka
har in ce, ‘Wane ne Ubangiji?’
Ko kuwa in zama matalauci in yi sata
ta haka in kunyata sunan Allahna.

10 “Kada ka baza ƙarairayi game da bawa ga maigidansa,
in ba haka ba, zai la’ance ka, za ka kuwa sha wahala a kan haka.

11 “Akwai waɗanda sukan zagi mahaifinsu
ba sa kuma sa wa mahaifiyarsu albarka;
12 waɗanda sukan ɗauka su tsarkaka ne a ganinsu
alhali kuwa ƙazamai ne su;
13 waɗanda kullum idanunsu masu kallon reni ne,
waɗanda kallon da suke yi na daurin gira ne;
14 waɗanda haƙoransu takuba ne
waɗanda kuma muƙamuƙansu tarin wuƙaƙe ne
don su cinye matalauta daga duniya
da kuma mabukata daga cikin mutane.

15 “Matsattsaku tana da ’ya’ya mata biyu.
Suna kuka suna cewa, ‘Ba ni! Ba ni!’

“Akwai abubuwa uku da ba sa taɓa ƙoshi,
guda huɗu ba sa taɓa cewa, ‘Ya isa!’
16 Kabari, mahaifar da ba ta haihuwa,
ƙasa, wadda ba ta taɓa ƙoshi da ruwa,
da kuma wuta, wadda ba ta taɓa cewa ‘Ya isa!’

17 “Idon da yake yi wa mahaifi ba’a,
wanda yake wa mahaifiya dariyar rashin biyayya,
hankakin kwari za su ƙwaƙule masa ido,
ungulai za su cinye su.

18 “Akwai abubuwa uku da suke ba ni mamaki,
abubuwa huɗu da ba na iya fahimtarsu,
19 yadda gaggafa take firiya a sararin sama,
yadda maciji yake tafiya a kan dutse,
yadda jirgin ruwa yake tafiya a teku,
da kuma sha’ani tsakanin namiji da ’ya mace.

20 “Ga yadda mazinaciya take yi.
Takan ci ta share bakinta
ta ce, ‘Ban yi wani abu marar kyau ba.’

21 “Akwai abubuwa uku da duniya kan yi rawan jiki,
abubuwa huɗu da ba ta iya jurewa,
22 bawan da ya zama sarki,
wawan da ya ƙoshi da abinci,
23 macen da ba a ƙauna wadda ta sami miji,
da kuma baiwar da ta ɗauki matsayin uwargijiyarta.

24 “Akwai abubuwa huɗu a duniya da suke ƙanana,
duk da haka suna da hikima ƙwarai.
25 Kyashi halittu ne da ba su da ƙarfi sosai,
duk da haka suna ajiyar abincinsu da rani;
26 remaye halittu ne da ba su da ƙarfi sosai,
duk da haka sukan yi gidajensu a duwatsu;
27 fāra ba su da sarki,
duk da haka suna tafiya tare bisa ga girma;
28 ana iya kama ƙadangare da hannu,
duk da haka akan same shi a fadodin sarakuna.

29 “Akwai abubuwa uku da suke jan jiki da kuma taƙama a tafiyarsu
abubuwa huɗu waɗanda suke kwarjini da taƙama a tafiyarsu,
30 zaki mai ƙarfi a cikin namun jeji, wanda ba ya ratse wa kowa;
31 zakara mai taƙama,
da bunsuru,
da kuma sarki mai sojoji kewaye da shi.

32 “In ka yi wauta ka kuma ɗaukaka kanka,
ko kuwa wani yana ƙulla maka mugunta,
ka dāfa hannunka a bisa bakinka!
33 Gama kamar yadda kaɗaɗɗen madara takan kawo mai,
murɗa hanci kuma takan sa a yi haɓo,
haka tsokanar fushi takan kawo faɗa.”

## Maganganun Sarki Lemuwel

# 31

1 Maganganun Sarki Lemuwel, magana ce horarriya* mahaifiyarsa ta koya masa,
2 “Ka saurara, ya ɗana! Ka saurara, ɗan cikina!
Ka saurara, ya ɗan amshin addu’ata!†
3 Kada ka ba da ƙarfinka a kan mata,
ƙarfinka ga waɗanda suka hallaka sarakuna.

* 31:1 Ko kuwa na Lemuwel sarkin Massa, waɗanda † 31:2 Ko kuwa / amsar addu’o’ina

4 “Ba na sarakuna ba ne, ya Lemuwel,
ba na sarakuna ba ne su sha ruwan inabi,
ba na masu mulki ba ne su yi marmarin barasa,
5 don kada su sha su manta da abin da doka ta umarta,
su hana wa waɗanda aka danne hakkinsu.
6 A ba da barasa ga waɗanda suke cikin halin ƙaƙa naka yi,
ruwan inabi ga waɗanda suke cikin wahala;
7 bari su sha su manta da talaucinsu
kada kuma su ƙara tunawa da ɓacin ransu.

8 “Yi magana domin bebaye,
domin hakkin dukan waɗanda suke naƙasassu.
9 Yi magana a kuma yi shari’ar adalci;
a tsare hakkin talakawa da masu bukata.”

## Maganar ƙarshe. Mace Mai Halin Kirki

10 ‡ Wa yake iya samun mace mai halin kirki?
Darajarta ta fi ta lu’ulu’ai.
11 Mijinta yana da cikakken amincewa da ita
kuma ba ya rasa wani abu mai daraja.
12 Takan yi masa alheri ba mugunta ba,
dukan kwanakin ranta.
13 Takan zaɓi ulu da lilin
ta yi ta saƙa da hannuwanta da farin ciki.
14 Ita kamar jirgin ’yan kasuwa ne
tana kawo abincinta daga nesa.
15 Takan farka tun da sauran duhu;
ta tanada wa iyalinta abinci
ta kuma shirya wa ’yan matan gidanta ayyukan da za su yi.
16 Takan lura da gona sosai ta kuma saye ta;
daga abin da take samu na kuɗin shiga take shuka gonar inabi.
17 Takan himmantu tă yi aikinta tuƙuru;
hannuwanta suna da ƙarfi domin ayyukanta.
18 Takan tabbata akwai riba a kasuwancinta,
kuma fitilarta ba ya mutuwa da dare.
19 Da hannunta take riƙe abin kaɗi
ta kuma kama abin saƙa da yatsotsinta.
20 Takan marabci talakawa
takan kuma taimaki masu bukata.
21 Sa’ad da ƙanƙara ta fāɗi, ba ta jin tsoro saboda gidanta;
gama dukansu suna da tufafi masu kauri.
22 Takan yi wa gadonta kayan shimfiɗa;
tufafinta kuma na lilin ne mai laushi na shunayya.
23 Ana girmama mijinta a ƙofar shiga birni
inda yakan zauna a cikin dattawan gari.
24 Takan yi riguna na lilin ta sayar;
takan kuma sayar wa ’yan kasuwa da ɗamara.
25 Karfi da mutunci su ne suturarta;
za tă iya yin dariyar kwanaki masu zuwa.
26 Tana magana da hikima,
kuma umarnai mai aminci yana a harshenta.

‡ **31:10** Ayoyi 10-31 suna bin juna layi-layi, kowace aya na farawa da harufan Ibraniyanci bi da bi.

27 Tana lura da sha’anin gidanta
kuma ba ta cin abincin ƙyuya.
28 ’Ya’yanta sukan tashi su ce da ita mai albarka;
haka mijinta ma, yakan kuma yabe ta yana cewa,
29 “Mata da yawa suna yin abubuwan yabo,
amma ke kin fi su duka.”
30 Kayan tsari yana ruɗu, kyau kuma kan shuɗe;
amma mace mai tsoron UBANGIJI abar yabo ce.
31 Ka ba ta ladar da ya dace tă samo wa kanta,
bari kuma ayyukanta su kawo mata yabo a ƙofar shiga birni.

# Mai Hadishi

*Kome ba shi da amfani*

1 Kalmomin Malami,* ɗan Dawuda, Sarki a Urushalima.
2 “Ba amfani! Ba amfani!”
In ji Malami.
“Gaba ɗaya ba amfani!
Kome ba shi da amfani!”

3 Wace riba ce mutum yake samu daga wahalar
da yake fama a duniya?
4 Zamanai sukan zo zamanai su wuce,
amma duniya tana nan har abada.
5 Rana takan fito rana ta kuma fāɗi,
ta kuma gaggauta zuwa inda takan fito.
6 Iska takan hura zuwa kudu ta kuma juya zuwa arewa;
tă yi ta kewayewa, tă yi ta koma inda take fitowa.
7 Dukan rafuffuka sukan gangara zuwa teku,
duk da haka teku ba ya cika.
Daga inda rafuffukan suke fitowa,
a can suke komawa kuma.
8 Dukan abubuwa suna kawo gajiya,
gaban magana.
Ido ba ya gaji da gani,
haka ma kunne yă ƙoshi da ji.
9 Abin da ya taɓa kasancewa, zai sāke kasance,
abin da aka yi za a sāke yi kuma;
babu wani abu sabo a duniya.
10 Akwai wani abin da za a ce,
“Duba! Ga wani abu sabo”?
Abin yana nan, tun dā can,
ya kasance kafin lokacinmu.
11 Ba a tunawa da mutanen dā,
haka su ma da ba a haifa ba tukuna
waɗanda za su biyo bayansu
ba za a tuna da su ba.

*Hikima ba ta da amfani*

12 Ni, Malami, sarki ne bisa Isra’ila a Urushalima. 13 Na dauri aniyata in gwada don
in bincika ta wurin hikima dukan abin da ake yi a duniya. Kaya mai nauyi ne Allah
ya ɗora a kan mutane! 14 Na ga dukan abubuwan da ake yi a duniya, dukansu ba su
da amfani, naushin iska ne kawai.
15 Abin da yake tanƙwararre ba zai miƙu ba;
ba za a kuma iya ƙidaya abin da ba shi ba.
16 Na yi tunani a raina na ce, “Duba, na yi girma, na kuma ƙaru da hikima fiye
da duk wanda ya taɓa mulki a bisa Urushalima kafin ni; na ɗanɗana hikima mai
yawa da kuma ilimi.” 17 Sa’an nan na ɗaura aniyata ga fahimtar hikima, in kuma

* **1:1** Ko kuwa shugaban taro; haka ma a ayoyi 2 da kuma 12.

san bambanci tsakanin hauka da wauta, amma na koyi cewa wannan ma, naushin
iska ne kawai.
18 Gama yawan hikima yakan kawo yawan baƙin ciki;
yawan sani, yawan ɓacin rai.

# 2

*Jin daɗi ba shi da amfani*

1 Na ce wa kaina, "Zo, zan gwada ka da jin daɗi don in ga abin da yake da kyau."
Amma wannan ma ya zama ba amfani. 2 Sai na ce, "Dariya hauka ce. Kuma me jin
daɗi yake kawowa?" 3 Na yi ƙoƙari in sa raina yă yi farin ciki da ruwan inabi, in
kuma rungumi wauta, hankalina kuma yana yin mini jagora da hikima. Na so in ga
abin da yake da daraja ga mutane a duniya a 'yan kwanakinsu.
4 Na yi ayyuka masu girma. Na gina gidaje wa kaina na kuma shuka gonakin
inabi. 5 Na yi lambuna da wuraren shaƙatawa, na shuka itatuwa masu 'ya'ya iri-iri
a cikinsu. 6 Na yi tankuna don in yi banruwan kurmin itatuwa. 7 Na sayi bayi mata
da maza, ina kuma da waɗansu bayin da aka haifa a gidana. Ina da garkunan shanu
da na tumaki da na awaki fiye da duk wanda ya taɓa zama a Urushalima kafin ni.
8 Na tara wa kaina azurfa da zinariya, ina da ma'ajin sarakuna da yankuna. Na samo
wa kaina mawaƙa mata da maza, da dukan irin matan da kowane namiji zai so.
9 Na ƙasaita fiye da kowane mutumin da ya riga ni zama a Urushalima. Cikin dukan
wannan, hikimata ba tă rabu da ni ba.
10 Ban hana kaina duk wani abin da idona ya yi sha'awarsa ba;
ban hana zuciyata wani jin daɗi ba.
Zuciyata ta yi murna da dukan aikina,
wannan kuwa shi ne ladan dukan famata.
11 Duk da haka sa'ad da na duba dukan aikin hannuwana,
da abin da na yi fama don in samu,
sai kome ya zama ba shi da amfani, naushin iska ne kawai;
babu wata riba a duniya.

*Hikima da wauta ba su da amfani*

12 Sai na juya ga tunanina don in lura da hikima,
da kuma hauka da wauta.
Me ya rage wa magājin sarki yă yi
fiye da abin da aka riga aka yi?
13 Na ga cewa hikima ta fi wauta,
kamar yadda haske ya fi duhu.
14 Mai hikima ya san inda ya nufa,
wawa kuwa yana tafiya a cikin duhu;
amma sai na gane
cewa ƙaddara ɗaya ce take samunsu.
15 Sai na yi tunani a zuciyata,
"Kaddarar wawa za tă same ni ni ma.
Wace riba ce hikimata za tă jawo mini?"
Na ce a zuciyata,
"Wannan ma ba shi da amfani."
16 Gama ba za a ƙara tunawa da mai hikima ko wawa ba;
nan gaba za a manta da su.
Yadda wawa zai mutu, haka ma mai hikima!

*Fama ba ta da amfani*

[17] Don haka na ƙi jinin rayuwa, gama aikin da ake yi a duniya yana ɓata mini rai.
Dukan abin da yake cikinta kuwa ba shi da amfani, naushin iska ne kawai. [18] Na
ƙi jinin dukan abubuwan da na yi wahala ina yi a duniya, gama dole in bar su wa
na bayana. [19] Wa ya sani ko zai zama mai hikima ko kuma wawa? Duk da haka
zai mallaki dukan aikin da na yi da ƙoƙarina da kuma dabarata a duniya. Wannan
ma ba shi da amfani. [20] Saboda haka zuciyata ta fara karaya a kan dukan faman
aikina a duniya. [21] Gama mutum zai yi aikinsa da dukan hikimarsa, da saninsa, da
gwanintarsa, sa'an nan dole yă bar dukan abin da ya mallaka ga wani wanda bai yi
wahalar kome a ciki ba. Wannan ma ba shi da amfani, hasara ce mai yawa. [22] Me
mutum zai samu daga aikin da ya yi duka, da irin ɗawainiyar da ya sha a kan yin
aikin a duniya? [23] Dukan kwanakinsa aikinsa damuwa ce da ɓacin zuciya; ko da dare
ma hankalinsa ba a kwance yake ba. Wannan ma ba shi da amfani.
[24] Ba abin da mutum zai yi da ya fi yă ci, yă sha, yă ji wa ransa daɗi daga aikinsa.
Na lura cewa wannan ma, ya fito daga hannun Allah ne, [25] gama in ba tare da shi
ba, wa zai iya ci yă sha yă kuma ji daɗi? [26] Ga wanda ya gamshe shi, Allah yakan
ba da hikima da sani da farin ciki, amma ga mai zunubi yakan ba shi aikin tarawa
da ajiyar dukiya domin yă miƙa wa wanda ya gamshi Allah. Wannan ma ba shi da
amfani, naushin iska ne kawai.

# 3

*Lokaci domin kowane abu*

[1] Akwai lokaci domin kowane abu,
da kuma lokaci domin kowane aiki a duniya.
[2] Lokacin haihuwa da lokacin mutuwa,
lokacin shuki da lokacin tumɓukewa.
[3] Lokacin kisa da lokacin warkarwa,
lokacin rushewa da lokacin ginawa.
[4] Lokacin kuka da lokacin dariya,
lokacin makoki da lokacin rawa.
[5] Lokacin warwatsa duwatsu da lokacin tara su,
lokacin runguma da lokacin dainawa.
[6] Lokacin nema, da lokacin fid da zuciya,
lokacin ajiyewa da lokacin zubarwa.
[7] Lokacin yagewa da lokacin ɗinkewa,
lokacin yin shiru da lokacin magana.
[8] Lokacin ƙauna da lokacin ƙiyayya,
lokacin yaƙi da lokacin salama.
[9] Wace riba ce ma'aikaci yake da ita saboda wahalarsa? [10] Na ga nawayar da Allah
ya ɗora a kan mutane. [11] Ya yi kowane abu da kyau a lokacinsa. Ya kuma sa matuƙa
a zukatan mutane, duk da haka sun kāsa gane abin da Allah ya yi daga farko zuwa
ƙarshe. [12] Na san ba abin da ya fi wa mutane kyau fiye da su ji daɗi su kuma yi alheri
yayinda suke da rai. [13] Cewa kowa yă ci, yă sha, yă kuma ji daɗi cikin dukan aikinsa,
wannan kyautar Allah ce. [14] Na san cewa duk abin da Allah ya yi zai dawwama har
abada; ba abin da za a ƙara ko a rage. Allah ya yi haka domin mutane su girmama
shi.
[15] Duk abin da yana nan ya taɓa kasancewa,
kuma abin da zai kasance, ya taɓa kasancewa;
Allah kuma zai nemi bayanin abubuwan da suka wuce.
[16] Sai na ga wani abu kuma a duniya,
a wurin shari'a, akwai mugunta a can,
a wurin adalci, akwai mugunta a can.

[17] Sai na yi tunani a zuciyata,
“Allah zai shari’anta
masu adalci da masu mugunta,
gama za a kasance da lokaci domin kowane aiki,
lokaci domin kowane abu.”
[18] Na sāke yin tunani, “Game da mutane kam, Allah kan gwada su don su san cewa
ba su fi dabba ba. [19] Kaddarar mutum ɗaya take da ta dabba; ƙaddara ɗaya ce take
jiransu biyu. Yadda ɗayan yake mutuwa, haka ma ɗayan. Dukansu numfashinsu iri
ɗaya ne; mutum bai fi dabba ba. Kowane abu ba shi da amfani. [20] Duka wuri ɗaya za
su tafi; gama duka daga turɓaya suka fito, kuma ga turɓaya duka za su koma. [21] Wa ya
tabbatar cewa ruhun mutum yakan tashi sama sa’an nan na dabba yă sauka ƙasa?”
[22] Saboda haka na ga babu abin da ya fi kyau wa mutum fiye da yă more wahalar
aikinsa, domin wannan ne rabonsa. Gama wa zai kawo shi yă ga abin da zai faru a
bayansa?

# 4

*Zalunci, wahalar aiki da rashin abokantaka*

[1] Na sāke dubawa sai na ga zaluncin da ake yi a duniya.
Na ga hawayen waɗanda ake zalunta
kuma ba su da mai taimako;
masu iko suna goyon bayan masu zalunci,
ga shi ba su da mai taimako.
[2] Sai na furta cewa matattu,
waɗanda suka riga suka mutu,
sun fi waɗanda suke a raye farin ciki,
waɗanda har yanzu suke da rai.
[3] Amma wanda ya fi su duka
shi ne wanda bai riga ya kasance ba,
wanda bai ga muguntar
da ake yi a duniya ba.
[4] Sai na gane cewa, duk wata fama da duk wata nasara sun samo asali daga kishin
da mutum yake yi na maƙwabcinsa ne. Wannan ma ba shi da amfani, naushin iska
ne kawai.
[5] Wawa yakan kame hannuwansa
yă kuma lalatar da kansa.
[6] Gara tafin hannu guda cike da kwanciyar rai
da tafin hannu biyu cike da tashin hankali
da harbin iska kawai.
[7] Na kuma ga wani abu marar amfani a duniya.
[8] Akwai wani mutum shi kaɗai;
bai shi da ɗa ko ɗan’uwa.
Ba shi da hutu daga wahalarsa,
duk da haka bai ƙoshi da dukiyarsa ba.
Ya tambayi kansa, “Ma wane ne nake wannan wahala,
kuma me ya sa nake hana kaina jin daɗi?”
Wannan ma ba shi da amfani,
harkar baƙin cikin ne kawai!

[9] Biyu sun fi ɗaya,
gama suna samun riba mai kyau na aikinsu.
[10] In ɗaya ya fāɗi,

abokinsa zai taimake shi yă tashi.
Amma abin tausayi ne ga mutumin da ya fāɗi
ba shi kuma da wanda zai taimake shi yă tashi!
11 In mutum biyu sun kwanta tare, za su ji ɗumin juna.
Amma yaya mutum ɗaya zai ji ɗumi yana shi kaɗai?
12 Ana iya shan ƙarfin mutum ɗaya,
mutum biyu za su iya kāre kansu.
Igiya riɓi uku tana da wuya tsinkawa.

### *Cin gaba ba shi da amfani*

13 Gara saurayi wanda yake matalauci amma yake da hikima da sarkin da ya tsufa
mai wauta, wanda ba ya karɓar shawara. 14 Yana yiwuwa saurayin yă fito daga
kurkuku yă hau gadon sarauta, ko kuma dai an haife shi cikin talauci a ƙasarsa.
15 Na ga cewa dukan waɗanda suka rayu suka kuma yi tafiya a duniya sun bi saurayin,
magājin sarkin. 16 Babu ƙarshe ga dukan mutanen da suka riga su. Amma waɗanda
suka zo daga baya, ba su gamsu da magājin ba. Wannan ma ba shi da amfani, naushin
iska ne kawai.

## 5

### *Ka ji tsoron Allah*

1 Ka lura da matakanka sa'ad da ka tafi gidan Allah. Ka je kusa don ka saurara a
maimakon miƙa hadaya kamar wawaye, waɗanda ba su san sun yi laifi ba.
2 Kada ka yi subul da bakinka,
kada zuciyarka tă yi garajen
furta wani abu a gaban Allah.
Allah yana sama
kai kuma kana duniya,
saboda haka, kada kalmominka su zama da yawa.
3 Kamar yadda son cika buri yakan zo sa'ad da kana da yawan damuwa,
haka jawabin wawa yake sa'ad da yake yawan magana.
4 Sa'ad da ka yi alkawari ga Allah, kada ka ɓata lokaci wajen cika shi. Ba ya jin
daɗin wawaye; ka cika alkawarinka. 5 Gara kada ka yi alkawari, da ka yi amma ba
ka cika ba. 6 Kada ka bar bakinka ya kai ga yin zunubi. Kada kuma ka kai ƙara wurin
ɗan saƙon haikali cewa, "Alkawarin da na yi kuskure ne." Me ya sa Allah yake fushi
a kan abin da ka faɗa har yă lalatar da aikin hannuwanka? 7 Yawan buri da yawan
magana ba su da amfani. Saboda haka, ka ji tsoron Allah.

### *Arziki ba shi da amfani*

8 In ka ga ana zaluntar matalauta a wani yanki, ba a yin adalci, ana kuma tauye
hakki, kada ka yi mamakin waɗannan abubuwa; domin akwai wani jami'in da yake
bisa da wani, a bisansu biyu kuwa akwai wani. 9 Kowa yakan amfana da bunkasar
amfanin ƙasa, sarki kansa yana samun riba daga gonaki.
10 Duk mai ƙaunar kuɗi ba ya samun isashe;
duk ma ƙaunar dukiya ba ya ƙoshi da abin da yake samu.
Wannan ma ba shi da amfani.

11 Kamar yadda kaya suke haɓaka,
haka ma masu amfani da su.
Kuma wane amfani ne suke ga mai shi
in ba ciyar da idanunsa a kansu ba?

12 Barcin ma'aikaci daɗi gare shi,
ko yă ci kaɗan ko da yawa,
amma yalwar mai arziki
ba ta barinsa yă iya yin barci.
13 Na ga wani mugun abu a duniya,
arzikin da aka ajiye don yă cuce mai shi,
14 ko kuwa dukiyar da ta ɓace ta wata hasara,
har ya zama sa'ad da ya haifi ɗa,
babu abin da ya bar masa.
15 Tsirara mutum yakan fito daga cikin mahaifiyarsa,
kuma kamar yadda ya fito, haka zai koma.
Ba ya ɗaukan kome daga wahalarsa
da zai riƙe a hannunsa.
16 Wannan ma mugun abu ne,
Yadda mutum ya zo, haka zai koma,
to, wace riba ce ya ci,
da yake ya yi wahalar iska ce kawai?
17 Duk rayuwarsa ya ci abinci a cikin duhu,
da ɓacin rai mai tsanani, da azaba, da fushi.
18 Sa'an nan na gane cewa abu mai kyau ne, daidai ne kuma mutum yă ci, yă sha,
yă kuma ji daɗin aikin da ya yi a 'yan kwanakin da Allah ya ba shi, gama wannan
shi aka ƙaddara wa mutum daga faman wahalarsa a duniya a cikin 'yan kwanakin
da Allah ya ba shi a duniya, gama wannan shi ne rabonsa. 19 Ban da haka ma, sa'ad
da Allah ya ba wa mutum dukiya da wadata, ya kuma ba shi zarafi yă ji daɗinsu, ya
kuma amince da rabonsa, sai yă ji daɗin aikinsa, wannan kyauta ce ta Allah. 20 Da
ƙyar yake tunani a kan kwanakin rayuwarsa, domin Allah ya yarje masa, yă zauna
da farin ciki.

# 6

1 Na ga wani mugun abu a duniya, ya kuma nawaita wa mutane ƙwarai. 2 Allah
yakan ba mutum dukiya, da wadata da kuma girma, don kada yă rasa abin da ransa
yake so, amma Allah bai ba shi zarafin more su ba, a maimakon haka ma sai baƙo
ne yă more su. Wannan ba shi da amfani, mugun abu ne ƙwarai.
3 Mutum zai iya kasance da 'ya'ya ɗari, yă kuma yi shekaru masu yawa; duk
da haka kome daɗewarsa, in bai more wadatarsa ba, bai kuma sami kyakkyawar
binnewa ba, na ce, gara wanda aka haife shi gawa. 4 Haihuwa ba tă amfane wanda
aka haifa gawa ba, gama ya zo daga duhu ya koma duhu inda aka manta da shi. 5 Ko
da yake bai ga hasken rana ba, bai kuma san kome ba, duk da haka ya dai huta, fiye
da mutumin da bai more wa ransa ba, 6 ko da ya yi shekara dubu biyu amma bai
more wadatarsa ba. Ba wuri ɗaya dukansu biyu za su tafi ba?
7 Dukan ƙoƙarin da mutum yake yi, yana yi ne domin bakinsa,
duk da haka bai taɓa gamsar da abin da yake marmari.
8 Da me mai hikima ya fi wawa?
Wace riba ce matalauci yakan samu don yă iya zama da mutane?
9 Gara abin da ido ya gani
da kwaɗayin da bai sami biyan bukata ba.
Wannan ma ba shi da amfani,
naushin iska ne kawai.

10 Duk abin da ya kasance, to, yana da suna,
kuma duk abin da mutum yake, an riga an sani.

Ba mutumin da zai iya ƙarawa
da wanda ya fi shi ƙarfi.
11 Yadda yawan magana take
haka ƙarancin amfaninta,
yaya wannan zai amfane wani?
12 Gama wa ya san abin da ya fi dacewa ga mutum a ʼyan kwanakinsa marasa
amfani da sukan wuce kamar inuwa? Wa kuma zai iya faɗa masa abin da zai faru a
duniya bayan ya rasu?

# 7

*Hikima*

1 Suna mai kyau ya fi turare mai ƙanshi,
kuma ranar mutuwa ta fi ranar haihuwa.
2 Gara a tafi gidan makoki
da a je gidan biki,
gama mutuwa ce ƙaddarar kowane mutum;
ya kamata masu rai su lura da haka.
3 Baƙin ciki ya fi dariya,
gama baƙin ciki yakan kawo gyara.
4 Zuciyar masu hikima tana a gidan makoki,
amma zuciya wawaye tana a gidan shagali.
5 Gara ka saurari tsawatawar mai hikima
da ka saurari waƙar wawaye.
6 Kamar ƙarar ƙayar da take karce gindin tukunya,
haka dariyar wawaye take.
Wannan ma ba shi da amfani.

7 Zalunci yakan mai da mutum mai hikima wawa,
cin hanci kuma yakan lalace hali.

8 Karshen abu ya fi farkonsa,
haƙuri kuma ya fi girman kai.
9 Kada ranka yǎ yi saurin tashi,
gama fushi yana zama a cinyar wawaye.

10 Kada ka ce, "Me ya sa kwanakin dā sun fi waɗannan?"
Gama ba daidai ba ne a yi irin waɗannan tambayoyi.

11 Hikima, kamar gādo, abu mai kyau ne
tana kuma da amfani ga waɗanda suka ga rana.
12 Hikima mafaka ce
takan kāre mutum kamar yadda kuɗi suke yi.
Kiyayewar da hikima takan yi wa mai ita
ita ce amfanin ilimi.
13 Ku lura da abin da Allah ya yi.
Wa zai iya miƙe
abin da ya tanƙware?
14 Saʼad da alʼamura suke tafiya daidai, ka yi farin ciki,
amma saʼad da suka lalace, ka tuna,
Allah ne ya yi wancan
shi ne kuma ya yi wannan.

Saboda haka, mutum ba zai san
wani abu game da nan gabansa ba.
15 A cikin rayuwan nan ta rashin amfani nawa, na lura da waɗannan abubuwa
biyu,
mai adalci yana hallakawa cikin adalcinsa,
mai mugunta kuma yana tsawon rai cikin muguntarsa.
16 Kada ka cika yin adalci, fiye da kima,
kada kuma ka cika yin hikima,
don me za ka hallaka kanka!
17 Kada ka cika yin mugunta,
kada kuma ka cika yin wauta,
don me za ka mutu kafin lokacinka?
18 Yana da kyau ka kama ɗaya
ba tare da ka saki wancan ba.
Mai tsoron Allah zai guji wuce gona da iri.*

19 Hikima takan sa mutum guda mai hikima yă yi ƙarfi
fiye da masu mulki goma a cikin birni.

20 Babu mai adalci a duniya
wanda yake yin abin da yake daidai da bai taɓa yin zunubi ba.

21 Kada ka mai da hankali ga dukan abin da mutane suke faɗi,
in ba haka ba wata rana za ka ji bayinka suna zaginka.
22 Gama kai kanka ka sani
cewa sau da yawa ka zagi waɗansu.
23 Dukan waɗannan na gwada su ta wurin hikima na kuma ce,
“Na ƙudurta in zama mai hikima,”
amma abin ya fi ƙarfina.
24 Ko da me hikima take,
Abin ya yi mana zurfi ƙwarai, yana da wuyar ganewa,
wa zai iya gane shi?
25 Saboda haka na mai da hankalina ga fahimi,
don in bincika in nemi hikima da yadda aka tsara abubuwa,
in kuma fahimci wawancin mugunta
da haukar wauta.

26 Sai na iske wani abin da ya fi mutuwa ɗaci
mace wadda take tarko ne,
wadda zuciyarta tarko ne
wadda kuma hannuwanta sarƙa ne.
Mutumin da ya gamshi Allah zai tsere mata,
amma za tă kama mai zunubi.
27 Malami ya ce, “Duba, abin da na gane ke nan.
“Na tara abu guda da wani, don in gane tsarin abubuwa,
28 yayinda nake cikin nema
amma ban samu ba,
sai na sami adali guda cikin dubu,
amma ba mace mai adalci guda a cikinsu duka.
29 Wannan ne kaɗai abin da na gane.
Allah ya yi mutum tsab

* **7:18** Ko kuwa zai bi su biyu

amma sai muka rikitar da kanmu.”

# 8

1 Wa yake kama da mai hikima?
Wa ya san bayanin abubuwa?
Hikima takan haskaka fuskar mutum,
ta kuma kawo sakin fuska.

*Ka yi wa sarki biyayya*

2 Ka yi biyayya da umarnin sarki, na ce, saboda alkawarin da ka yi a gaban Allah.
3 Kada ka yi hanzarin tashi daga gaban sarki. Kada ka kāre abin da ba daidai ba,
gama zai iya yin duk abin da ya ga dama. 4 Da yake maganar sarki ita ce mafificiya,
wa zai iya ce masa, “Me kake yi?”
5 Duk wanda ya yi biyayya da umarninsa ba zai sami lahani ba,
zuciya mai hikima kuma zai san lokacin da ya dace da kuma hanyoyin da suka fi.
6 Gama akwai lokaci da hanyoyin da suka dace da yin kowane abu,
ko da yake wahalar mutum ta yi masa yawa.

7 Da yake ba wanda ya san nan gaba,
wa zai iya faɗa masa abin da zai faru?
8 Ba wanda yake da iko a kan iska har da zai riƙe ta,
saboda haka babu mai iko kan ranar mutuwarsa.
Kamar yadda ba a sallamar mutum a lokacin yaƙi,
haka ma mugunta ba za tă saki masu aikata ta ba.

9 Na ga dukan waɗannan, yayinda na lura da kowane abin da ake yi a duniya.
Akwai lokacin da mutum yakan nauyaya wa waɗansu ba da sonsa ba. 10 Sa’an nan
kuma, na ga an binne masu mugunta, waɗanda suke shiga da fita daga tsattsarkan
wuri suke kuma samun yabo a birnin da suka yi wannan. Wannan ma ba shi da
amfani.
11 In ba a hanzarta aka yanke hukunci a kan laifi ba, zukatan mutane sukan cika
da ƙulle-ƙullen aikata abubuwan da ba daidai ba. 12 Ko da yake mugu ya aikata laifi
ɗari ya kuma yi tsawon rai, na san cewa zai fi wa masu tsoron Allah kyau, waɗanda
suke girmama Allah. 13 Duk da haka, domin masu mugunta ba su ji tsoron Allah ba,
abubuwa ba za su yi musu kyau ba, ransu kamar inuwa yake ba zai yi tsawo ba.
14 Akwai kuma wani abu marar amfani da yake faruwa a duniya, masu adalci
sukan sha hukuncin da ya dace da masu mugunta, masu mugunta kuma sukan karɓi
sakayyar da ya cancanci masu adalci su samu. Na ce, wannan ma, ba shi da amfani.
15 Saboda haka abin da na ce, shi ne mutum yă ji daɗi, domin iyakar jin daɗinsa a
wannan rai, shi ne yă ci, yă sha, yă ji wa kansa daɗi. Aƙalla yana iya yin wannan in
ya yi aiki a kwanakin da Allah ya ba shi a wannan duniya.
16 Da na mai da hankalina don in sami hikima in kuma lura da wahalar mutum
a duniya, ko da a ce idanunsa ba sa barci dare da rana, 17 sam, ba zai taɓa fahimci
abin da Allah yake yi ba. Iyakar ƙoƙarin da ka yi duk ba za ka iya ganewa ba. Masu
hikima suna iya cewa sun sani, amma kuwa ba su sani ba.

# 9

*Makoma ɗaya ce ga kowa*

1 Sai na yi tunani a kan wannan na kuma gane cewa masu adalci da masu hikima
da kuma abubuwan da suke yi suna a hannun Allah ne, amma ba wanda ya san
ko ƙauna ko ƙiyayya ce take jiransa. 2 Dukansu makomarsu ɗaya ce, masu adalci

da masu mugunta, masu kirki da marasa kirki, masu tsabta da marasa tsabta, masu
miƙa hadaya da waɗanda ba sa yi.

Kamar yadda yake ga mutumin kirki,
haka yake ga mai zunubi.
Kamar yadda yake ga masu yin rantsuwa,
haka ma da masu tsoron yi.

3 Wannan ita ce muguntar da take faruwa a cikin dukan abubuwa a duniya.
Kaddara ɗaya ce take a kan kowa. Amma zukatan mutane cike suke da mugunta,
akwai kuma hauka a zukatansu yayinda suke a raye, bayan haka kuma sai su mutu.
4 Duk wanda yake da rai a wannan duniya ta rayayyu, yana sa zuciya, gara rayayyen
kare da mataccen zaki!

5 Gama rayayyu sun san za su mutu,
amma matattu ba su san kome ba;
ba su da wata lada nan gaba
an manta da su ke nan gaba ɗaya.
6 Kaunarsu, ƙiyayyarsu,
da kuma kishinsu tuni sun ɓace;
ba za su taɓa zama sashen
wani abin da yake faruwa a duniya ba.

7 Yi tafiyarka, ka ci abincinka da farin ciki, ka sha ruwan inabinka da farin zuciya,
gama abin da ka yi duka daidai ne a wurin Allah. 8 Kullum ka kasance cikin farin
riguna, ka kuma shafe kanka da mai kullum, 9 Ka more rayuwa da matarka, wadda
kake ƙauna, dukan kwanakin nan marasa amfani da Allah ya ba ka a duniya. Gama
wannan ne rabonka a rayuwa da kuma na faman aikinka a duniya. 10 Duk abin da
hannunka yake yi, ka yi shi da dukan ƙarfinka, gama a cikin kabari in da za ka, babu
aiki ko shirye-shirye, ko sani, ko hikima.

11 Na kuma ga wani abu a duniya.

Ba kullum maguji ne yake nasara a tsere ba,
ba kullum jarumi ne yake yin nasara ba,
ba kullum mai hikima ne da abinci ba
ba kullum mai basira ne yake da wadata ba
ba kullum gwani ne yake samun tagomashi ba;
amma sa'a, da tsautsayi, sukan sami kowannensu.

12 Ban da haka ma, ba wanda ya san sa'ad da lokacin mutuwarsa zai yi.

Kamar yadda akan kama kifi a muguwar raga,
ko a kama tsuntsu a tarko,
haka mugun lokaci yakan auko wa mutane, ba tsammani.

### *Hikima ta fi wauta*

13 Na kuma ga wani misali game da hikima a duniya wanda ya burge ni sosai.
14 An yi wani ɗan ƙaramin birni mai mutane kaɗan a ciki. Sai wani babban sarki
ya kawo masa yaƙi, ya kafa masa babban sansani. 15 A cikin birnin nan kuwa akwai
wani mutum matalauci amma mai hikima, ya kuma ceci birnin ta wurin hikimarsa.
Amma ba wanda ya tuna da matalaucin nan. 16 Sai na ce, "Hikima ta fi ƙarfe ƙarfi."
Amma aka rena hikimar matalaucin, ba a ma jin maganarsa.

17 Raɗar mai hikima da aka saurara cikin natsuwa
ta fi ihun mai mulkin wawaye.
18 Hikima ta fi kayan yaƙi,
amma mai zunubi ɗaya yakan rushe alheri mai yawa.

# 10

1 Kamar yadda matattun ƙudaje sukan ɓata ƙanshin turare,
haka ʼyar wauta takan ɓata hikima da daraja.
2 Zuciyar mai hikima takan karkata ga yin abin da yake daidai,
amma zuciyar wawa takan karkata ga yin mugun abu.
3 Ko yayinda yake tafiya a kan hanya
wawa yakan nuna cewa ba shi da hankali,
yakan nuna wa kowa wawancinsa.
4 In hankalin mai mulki ya tashi game da kai,
kada ka bar inda kake,
gama kwantar da hankali yakan sa a yafe manyan laifofi.

5 Akwai muguntar da na gani a duniya,
irin kuskuren da yake fitowa daga masu mulki.
6 Akan sa wawaye a manyan matsayi,
yayinda masu arziki suna ƙarƙashi.
7 Na taɓa ganin bayi a kan dawakai,
yayinda ʼyaʼyan sarki suna takawa a ƙasa kamar bayi.

8 Duk wanda ya haƙa rami shi ne zai fāɗa a ciki;
duk wanda ya rushe katanga, shi maciji zai sara.
9 Duk mai farfasa duwatsu shi za su yi wa rauni;
duk mai faskaren itace yana cikin hatsarinsu.

10 In gatari ya dakushe
ba a kuma wasa shi ba,
dole a yi amfani da ƙarfi da yawa,
amma ƙwarewa yana kawo nasara.

11 In maciji ya sari mutum kafin a ba shi makarin gardi,
ina amfanin maganin?

12 Kalmomi daga bakin mai hikima alheri ne,
amma maganganun wawa za su hallaka shi.
13 Farkon maganarsa wauta ce,
ƙarshenta kuma takan zama muguwar hauka,
14 wawa kuma yakan yi ta surutu.

Ba wanda ya san abin da zai zo
wa zai iya faɗa masa abin da zai faru bayan rasuwarsa?

15 Aikin wawa yakan gajiyar da shi,
har bai san hanyar zuwa gari ba.

16 Kaitonki, ya ke ƙasa wadda sarkinki bawa ne*
wadda kuma hakimanta ke ta shagali tun da safe.
17 Mai albarka ce, ya ke ƙasa wadda sarkinki haifaffen gidan sarauta ne,
wadda hakimanta suke samun abincinsu a daidai lokacin
don samun ƙarfi ba don buguwa ba.

* **10:16** Ko kuma sarki yaro ne

18 In mutum rago ne, sai tsaiko yă lotsa,
in hannuwansa ba masa yin kome, ɗaki yakan yi yoyo.

19 Akan shirya abinci don jin daɗi,
ruwan inabi kuwa don faranta zuciya,
amma kuɗi ne amsar kome.

20 Kada ka zagi sarki ko da a cikin tunaninka ne,
ko ka zagi mai arziki ko da a ɗakin kwananka ne,
gama tsuntsun sararin sama zai iya ɗauki maganarka,
tsuntsu mai fikafikai zai sanar da abin da ka ce.

# 11

*Burodi a bisa ruwaye*

1 Ka jefa burodinka a bisa ruwaye,
gama bayan kwanaki masu yawa, za ka sāke samunsa.
2 Ka raba abin hannunka ga mutum bakwai, I, har ma takwas,
gama ba ka san bala'in da zai auko wa ƙasar ba.

3 In gizagizai sun cika da ruwa,
sukan zub da ruwan sama bisa duniya.
Itace ya fāɗi, ko wajen kudu ne, ko wajen arewa,
inda ya fāɗi a nan zai kwanta.
4 Duk mai la'akari da iska, ba zai yi shuka ba,
mai la'akari da gizagizai kuma, ba zai yi girbi ba.

5 Kamar yadda ba ka san hanyar iska ba,
ko yadda aka siffanta jiki a cikin mahaifiya,
haka ba za ka fahimci aikin Allah
Mahaliccin dukan abubuwa ba.

6 Ka shuka irinka da safe,
da yamma kuma kada ka janye hannunka,
gama ba ka san wanda zai yi albarka ba,
ko wannan ko wancan,
ko kuma duka biyunsu su yi albarka.

*Ka tuna da mahaliccinka a ƙuruciyarka*

7 Haske da yana da kyau,
abu mai kyau ne kuma idanu su dubi rana.
8 Kome tsawon rayuwar mutum,
bari yă more su duka.
Amma bari kuma yă tuna da kwanakin duhu,
gama su ma za su yi yawa.
Duk abin da zai faru ba shi da amfani.

9 Ka yi murna, kai matashi, a ƙuruciyarka,
bari zuciyarka kuma tă yi farin ciki a kwanakin ƙuruciyarka.
Ka bi shawarar zuciyarka
da kuma duk abin da idanunka suka gani,
amma ka sani fa, cikin dukan al'amuran nan
Allah zai shari'anta ka.

10 Saboda haka, ka fid da tsoro daga zuciyarka
ka kakkaɓe duk wani abin da ya dami rayuwarka,
gama ƙuruciya da ƙarfi ba su da amfani.

# 12

1 Ka tuna da Mahaliccinka
a kwanakin ƙuruciyarka,
kafin lokacin wahala ta zo
shekaru kuma su ƙarato sa'ad da za ka ce,
"Ba na jin daɗinsu,"
2 kafin rana da haske
wata da taurari su daina haske,
gizagizai kuma su tattaru bayan da suka sheƙa ruwa;
3 sa'ad da masu tsaron gida suke rawar jiki,
majiya ƙarfi kuma suka rasa ƙarfi,
sa'ad da masu niƙa suka daina don ba su da yawa,
idanun da suke duba ta taga suka duhunta;
4 sa'ad da aka rufe ƙofofin shiga tituna
ƙarar niƙa kuma ya tsagaita;
sa'ad da kukan tsuntsaye ta farkar da mutane,
ba a kuwa jin waƙoƙinsu,
5 sa'ad da mutane suke jin tsoron tudu
da kuma hatsarori a tituna;
sa'ad da itacen almon ya toho,
fāra kuma ya yi ta jan jikinsa da ƙyar,
sha'awace-sha'awace sun kafe.
Daga nan mutum ya tafi madawwamiyar gidansa
ya bar masu makoki suna ta yi.

6 Ka tuna da shi, kafin igiyar azurfa ta katse,
ko tasar zinariya ta fashe;
kafin tulu yă ragargaje a maɓulɓula,
ko guga ta tsinke a rijiya,
7 turɓaya ta koma ƙasar da ta fito,
rai kuma yă koma ga Allah wanda ya ba da shi.

8 "Ba amfani! Ba amfani!" In ji Malami,
"Gaba ɗaya ba amfani!"

*Karshen magana*

9 Ba kawai Malami ya kasance mai hikima ba, amma kuma ya koyar da mutane.
Ya yi tunani ya kuma yi binciken da ya tsara karin magana masu yawa. 10 Malami
ya yi bincike don yă sami kalmomin da suka dace, kuma abin da ya rubuta daidai ne
da kuma gaskiya.
11 Kalmomin masu hikima kamar tsinken tsokanar dabba ne, tarin maganganunsu
kuma kamar ƙusoshi ne da aka kafa daram, da aka ba wa Makiyayi guda. 12 Ka yi
hankali ɗana, game da duk wani ƙari a kan waɗannan.

Wallafa littattafai ba shi da iyaka, kuma yawan karatu yakan gajiyar da jiki.

13 Yanzu an ji kome;
ga ƙarshen magana.
Ka ji tsoron Allah ka kuma kiyaye umarnansa,

gama wannan shi ne dukan hakkin mutum.
14 Gama Allah zai shari'anta kowane irin aiki,
har da waɗanda aka yi a ɓoye,
ko nagari ne, ko mugu.

# Waƙar Waƙoƙi

1 Waƙar Waƙoƙin Solomon.

*Kaunatacciya**
2 Bari yă sumbace ni da sumbar bakinsa,
gama ƙaunarka ta fi ruwan inabi zaƙi.
3 Kanshin turarenka mai daɗi ne;
sunanka kuwa kamar turaren da aka tsiyaye ne.
Shi ya sa mata suke ƙaunarka!
4 Ka ɗauke ni mu gudu, mu yi sauri!
Bari sarki yă kai ni gidansa.
*Kawaye*
Muna farin ciki muna kuma murna tare da kai,
za mu yabi ƙaunarka fiye da ruwan inabi.
*Kaunatacciya*
Daidai ne su girmama ka!

5 Ni baƙa ce, duk da haka kyakkyawa.
Ya ku 'yan matan Urushalima,
ni baƙa ce kamar tentunan Kedar,
kamar labulen tentin Solomon.†
6 Kada ku harare ni domin ni baƙa ce,
gama rana ta dafa ni na yi baƙa.
'Ya'yan mahaifiyata maza sun yi fushi da ni
suka sa ni aiki a gonakin inabi;
na ƙyale gonar inabi na kaina.
7 Faɗa mini, kai da nake ƙauna, ina kake kiwon garkenka
kuma ina kake kai tumakinka su huta da tsakar rana.
Me ya sa zan kasance kamar macen da aka lulluɓe
kusa da garkunan abokanka?
*Kawaye*
8 Ke mafiya kyau a cikin mata, in ba ki sani ba,
to, ki dai bi labin da tumaki suke bi
ki yi kiwon 'yan awakinki
kusa da tentunan makiyaya.
*Kaunatacce*
9 Ina kwatanta ke ƙaunatacciyata, da goɗiya
mai jan keken yaƙin kayan Fir'auna.
10 'Yan kunne sun ƙara wa kumatunki kyau,
wuyanki yana da jerin kayan wuya masu daraja.
11 Za mu yi 'yan kunnenki na zinariya,
da adon azurfa.
*Kaunatacciya*
12 Yayinda sarki yake a teburinsa,
turarena ya bazu da ƙanshi.

---

* **1:1** Da farko dai an nuna masu magana ko namiji ko ta mace bisa ga jinsi na wakilan sunayen da Ibraniyanci suka yi amfani da su, a gefen shafi ta wurin salon Kaunatacce da Kaunatacciya daki-daki. An nuna sauran kalmomin da Abokai. A waɗansu wurare akwai shakka game da ɓangarori da salo. † **1:5** Ko kuwa Salma

13 Kaunataccena yana kamar ƙanshin mur a gare ni,
kwance a tsakanin ƙirjina.
14 Kaunataccena kamar tarin furanni jeji ne gare ni
daga gonakin inabin En Gedi.

*Kaunatacce*

15 Ke kyakkyawa ce, ƙaunatacciyata!
Kai, ke kyakkyawa ce!
Idanunki kamar na kurciya ne.

*Kaunatacciya*

16 Kai kyakkyawa ne, ƙaunataccena!
Kai, kana ɗaukan hankali!
Gadonmu koriyar ciyawa ce.

*Kaunatacce*

17 Al'ul su ne ginshiƙan gidanmu;
fir su ne katakan rufin gidanmu.

# 2

*Kaunatacciya**

1 Ni furen bi-rana ne na Sharon,
furen bi-rana na kwari.

*Kaunatacce*

2 Kamar furen bi-rana a cikin ƙayayyuwa
haka ƙaunatacciyata take a cikin 'yan mata.

*Kaunatacciya*

3 Kamar itacen gawasa a cikin itatuwan jeji
haka ƙaunataccena yake a cikin samari.
Ina farin ciki in zauna a inuwarsa,
'ya'yan itacensa suna da daɗin ɗanɗanon da nake so
4 Ya kai ni babban zauren da ake liyafa,
ƙauna ita ce tutarsa a gare ni.
5 Ka ƙarfafa ni da zabibi
ka wartsake ni da gawasa,
gama ina suma don ƙauna.
6 Hannunsa na hagu yana a ƙarƙashin kaina,
hannunsa na dama kuma ya rungume ni.
7 'Yan matan Urushalima, ku yi mini alkawari
da bareyi da ƙishimai na jeji.
Ba za ku tā da ko ku farka ƙauna ba
sai haka ya zama lalle.

8 Saurara! Kaunataccena!
Duba! Ga shi ya iso,
yana tsalle a duwatsu,
yana rawa a bisa tuddai.
9 Kaunataccena yana kama da barewa ko sagarin ƙishimi
Duba! Ga shi can tsaye a bayan katangarmu,
yana leƙe ta tagogi,
yana kallo ta cikin asabari.
10 Kaunataccena ya yi magana ya ce mini,
"Tashi, ƙaunatacciyata,
kyakkyawata, ki zo tare da ni.

* **2:** Ko kuma Kaunatacce

11 Duba! Damina ta wuce;
ruwan sama ya ɗauke ya kuma ƙare.
12 Furanni sun hudo a duniya;
lokaci yin waƙa ya zo,
ana jin kukan kurciyoyi
ko'ina a ƙasarmu.
13 Itacen ɓaure ya fid da 'ya'yansa da sauri;
tohon inabi suna ba da ƙanshinsu.
Tashi, zo, ƙaunatacciyata;
kyakkyawata, zo tare da ni."

*Kaunataccena*

14 Kurciyata a kogon dutse,
a wuraren ɓuya a gefen dutse,
nuna mini fuskarki,
bari in ji muryarki;
gama muryarki da daɗi take,
fuskarki kuma kyakkyawa ce.
15 Kama mana ɓeraye,
ƙananan ɓerayen
da suke lalatar da gonakin inabi,
gonakin inabinmu da suke cikin yin fure.

*Kaunatacciya*

16 Kaunataccena nawa ne ni kuma tasa ce;
yana kiwon garkensa a cikin furannin bi-rana.
17 Sai gari ya waye
inuwa kuma ta watse,
ka juye, ƙaunataccena,
ka zama kamar barewa
ko kamar sagarin ƙishimi
a kan tuddai masu ciyawa.

# 3

1 Dare farai a kan gadona
na nemi wanda zuciyata take ƙauna;
na neme shi amma ban same shi ba.
2 Zan tashi yanzu in zagaya gari,
in ratsa titunansa da dandalinsa;
zan nemi wanda zuciyata take ƙauna.
Saboda haka na neme shi, amma ban same shi ba.
3 Masu tsaro suka gamu da ni
yayinda suke kai kawo a cikin birni, sai na ce,
"Kun ga mini wanda zuciyata take ƙauna?"
4 Rabuwata da su ke nan
sai na sami wanda zuciyata take ƙauna.
Na riƙe shi, ban yarda yǎ tafi ba
sai da na kawo shi gidan mahaifiyata,
zuwa ɗakin wadda ta yi cikina.
5 'Yan matan Urushalima, ku yi mini alkawari
da bareyi da ƙishimai na jeji.
Ba za ku tā da ko ku farka ƙauna ba
sai haka ya zama lalle.

6 Wane ne wannan mai zuwa daga hamada
kamar tunnuƙewar hayaƙi,
cike da ƙanshin turaren mur da lubban
da aka yi da kayan yajin 'yan kasuwa?
7 Duba! Abin ɗaukar Solomon ne,
jarumawa sittin suke rakiya,
zaɓaɓɓun sojojin Isra'ila,
8 dukansu suna saye da takobi
dukansu ƙwararru ne a yaƙi,
kowanne da takobinsa a rataye a gefensa,
a shirye don abubuwan bantsoro na dare.
9 Sarki Solomon ya yi wa kansa abin ɗauka;
ya yi shi da katako daga Lebanon.
10 An yi sandunansa da azurfa,
aka yi ƙasarsa da zinariya.
An lulluɓe wurin zaman da zanen shunayya,
'yan matan Urushalima sun yi mata irin yayen da ake yi na ƙauna.
11 Fito, ku 'yan matan Sihiyona,
ku ga Sarki Solomon yana saye da rawani,
rawanin da mahaifiyarsa ta naɗa masa,
a ranar aurensa,
a ranar da zuciyarsa ta yi farin ciki.

# 4

*Kaunatacce*
1 Ke kyakkyawa ce, ƙaunatacciyata!
Kai, ke kyakkyawa ce!
Idanunki sun yi kamar na kurciya a cikin lulluɓinki.
Gashinki ya yi kamar garken awaki
da suke gangarawa daga Dutsen Gileyad.
2 Haƙoranki sun yi kamar garken tumakin da ba a daɗe da yin musu sausaya ba,
da suke haurawa daga inda aka yi musu wanka.
Kowanne yana tare da ɗan'uwansa;
babu waninsu da yake shi kaɗai.
3 Leɓunanki kamar zaren jan garura
bakinki yana da kyau.
Kumatunki sun yi kamar rumman
da aka tsaga biyu a cikin lulluɓinki.
4 Wuyanki ya yi kamar hasumiyar Dawuda,
da aka gina da daraja;
a kansa an rataye garkuwoyi dubu,
dukansu garkuwoyin jarumawa ne.
5 Nonanki biyu sun yi kamar bareyi biyu,
kamar tagwayen barewa
da suke kiwo a cikin furen bi-rana.
6 Sai gari ya waye
inuwa kuma ta watse,
zan je dutsen mur
da kuma tudun turare.
7 Duk, ke kyakkyawa ce, ƙaunatacciyata;
babu wani lahani a cikinki.

8 Ki tare da ni daga Lebanon, amaryata,
zo tare da ni daga Lebanon.
Ki gangara daga ƙwanƙolin Amana,
daga ƙwanƙolin Senir, ƙwanƙolin Hermon,
daga ramin zaki
da kuma dutsen da damisoshi suke zama.
9 Kin saci zuciyata, ʼyarʼuwata, amaryata;
kin saci zuciyata
da hararar idanunki,
da dutse mai daraja guda na abin wuyanki.
10 Kaunarki abar farin ciki ne, ʼyarʼuwata, amaryata!
Kaunarki ta fi ruwan inabi gamsuwa,
ƙanshin turarenki kuma ya fi duk wani kayan yaji!
11 Leɓunanki suna zub da zaƙi kamar kakin zuma, amaryata;
madara da zuma suna a ƙarƙashin harshenki.
Kanshin rigunanki ya yi kamar na Lebanon.
12 Ke lambu ne da aka kulle, ʼyarʼuwata, amaryata;
ke maɓulɓula ce da aka kewaye, maɓulɓular da aka rufe.
13 Shuke-shukenki gonar rumman ne
da ʼyaʼyan itace masu kyau
na lalle da nardi,
14 nardi, da asfaran,
kalamus, da kirfa,
da kowane irin itacen turare,
da mur da aloyes
da kuma dukan kayan yaji masu kyau.
15 Ke lambun maɓulɓula ne,
rijiya mai ruwan da yake gudu
yana gangarawa daga Lebanon.

*Kaunatacciya*

16 Farka, iskar arewa,
ki kuma zo, iskar kudu!
Hura a kan lambuna,
don ƙanshinsa yă bazu har waje.
Bari ƙaunataccena yă zo cikin lambunsa
yă ɗanɗana ʼyaʼyan itacensa mafi kyau.

# 5

*Kaunatacce*

1 Na zo lambuna, ʼyarʼuwata, amaryata;
na tattara mur nawa da kayan yajina.
Na sha zumana da kuma kakinsa
na sha ruwan inabina da kuma madarana.

*Kawaye*

Ku ci, ku kuma sha, ya ku ƙawaye;
ku sha ku ƙoshi, ya ƙaunatattu.

*Kaunatacciya*

2 Na yi barci amma zuciyata tana a farke.
Ku saurara! Kaunataccena yana ƙwanƙwasa ƙofa.
“Buɗe mini, ʼyarʼuwata, ƙaunatacciyata,
kurciyata, marar laifina.
Kaina ya jiƙe da raɓa,

gashina ya yi danshin ɗiɗɗigar dare."
3 Na tuɓe rigata,
sai in sāke sa ta kuma?
Na wanke ƙafafuna,
sai in sāke ɓata su?
4 Kaunataccena ya turo hannunsa ta cikin ramin ƙofar;
zuciyata ta fara juyayi a kansa.
5 Na tashi don in buɗe wa ƙaunataccena,
sai hannuna ya jiƙe sharkaf da mur,
yatsotsina suna ɗiga da mur,
a hannuwan ƙofar.
6 Na buɗe wa ƙaunataccena ƙofa,
amma ƙaunataccena ba ya nan, ya riga ya tafi.
Zuciyata ta damu da tafiyarsa.
Na neme shi amma ban same shi ba.
Na yi ta kiransa amma bai amsa ba.
7 Masu gadi suka gamu da ni
yayinda suke kai kawo a cikin birni.
Suka yi mini dūka, suka yi mini rauni;
suka ƙwace gyalena
waɗannan masu gadin katanga!
8 'Yan matan Urushalima, ina roƙonku,
in kun sami ƙaunataccena
me za ku ce masa?
Ku ce masa na suma saboda ƙauna.
*Kawaye*
9 Mafiya kyau a cikin mata
me ya sa ƙaunataccenki ya fi sauran?
Don me kike roƙonmu mu faɗa masa yadda kike ji?
*Kaunatacciya*
10 Kaunataccena kyakkyawa ne ƙaƙƙarfa kuma,
da ƙyar a sami irinsa ɗaya a cikin dubu goma.
11 Kansa zinariya ce zalla;
gashinsa dogaye ne
baƙi wuluk kamar hankaka.
12 Idanunsa sun yi kamar na kurciyoyin
da suke kusa da ruwan rafi,
da aka wanke da madara
aka kuma kafa kamar kayan ado masu daraja.
13 Kumatunsa kamar lambun kayan yaji
suna ba da turare.
Leɓunansa sun yi kamar furen bi-rana
suna ɗiga da mur.
14 Hannuwansa kamar sandunan zinariyar
da aka sa musu duwatsu masu daraja.
Jikinsa ya yi kamar gogaggen hauren giwan
da aka yi masa ado da duwatsun saffaya.
15 Kafafunsa sun yi kamar ginshiƙan dutsen alabastar
da aka kafa su a cikin rammukar zinariya.
Kamanninsa ya yi kamar Lebanon,
mafi kyau kamar itacen al'ul nasa.
16 Bakinsa zaƙi ne kansa;

komensa yana da kyau.
Haka ƙaunataccena, abokina, yake
'yan matan Urushalima.

# 6

*Kawaye*

1 Ina ƙaunataccenki ya tafi,
yake mafiya kyau cikin mata?
Wace hanya ce ƙaunataccenki ya bi,
don mu taimake ki nemansa.

*Kaunatacciya*

2 Kaunataccena ya gangara zuwa lambunsa,
zuwa inda fangulan kayan yaji suke,
don yă yi kiwo a cikin lambun
don kuma yă tattara furen bi-rana.
3 Ni na ƙaunataccena ce, ƙaunataccena kuma nawa ne;
yana kiwo a cikin furen bi-rana.

*Kaunatacce*

4 Ke kyakkyawa ce, ƙaunatacciyata, kamar Tirza,
kyakkyawa kuma kamar Urushalima,
mai daraja kamar mayaƙa da tutoti.
5 Ki kau da idanu daga gare ni;
gama suna rinjayata.
Gashinki yana kama da garken awakin
da suke gangarawa daga Gileyad.
6 Haƙoranki suna kama da garken tumakin
da suke haurawa daga inda aka yi musu wanka.
Kowanne yana tare da ɗan'uwansa;
babu waninsu da yake shi kaɗai.
7 Kumatunki sun yi kamar rumman
da aka tsaga biyu a cikin lulluɓinki.
8 Sarauniyoyi sittin za su iya kasance a can,
da ƙwarƙwarai tamanin
da kuma budurwai da suka wuce ƙirge;
9 amma kurciyata, cikakkiyata, dabam take,
tilo kuwa ga mahaifiyarta,
'yar lele ga wadda ta haife ta.
'Yan mata sun gan ta suka ce da ita mai albarka;
sarauniyoyi da ƙwarƙwarai sun yabe ta.

*Kawaye*

10 Wace ce wannan da ta bayyana sai ka ce ketowar alfijir?
Kyakkyawa kamar wata, mai haske kamar rana,
mai daraja kamar taurari a jere?

*Kaunatacce*

11 Na gangara zuwa cikin itatuwan almon
don in ga ƙananan itatuwan da suke girma a kwari,
don in ga ko inabi sun yi 'ya'ya
ko rumman suna fid da furanni.
12 Kafin in san wani abu,

sha'awarta ta sa ni a cikin keken yaƙin sarkin mutanena.*

*Kawaye*

13 Ki dawo, ki dawo, ya Bashulammiya;
ki dawo, ki dawo, don mu dube ki!

*Kaunatacce*

Don me kuke duban Bashulammiya
sai ka ce rawar Mahanayim?

# 7

1 Kafafunki a cikin takalma kyakkyawa ne,
Ya diyar sarki!
Tsarin ƙafafunki sun yi kamar kayan ado masu daraja,
aikin hannun gwanin sassaƙa.
2 Cibinki kamar kwaf ne
da bai taɓa rasa gaurayayyen ruwan inabi ba.
Kwankwasonki ya yi kamar damin alkama
wanda furen bi-rana ya kewaye.
3 Nonanki sun yi kamar bareyi biyu,
tagwayen barewa.
4 Wuyanki ya yi kamar hasumiyar hauren giwa.
Idanunki sun yi kamar tafkin Heshbon
kusa da ƙofar Bat Rabbim.
Hancinki ya yi kamar hasumiyar Lebanon
wadda take duban Damaskus.
5 Kanki ya yi miki rawani kamar Dutsen Karmel.
Gashinki ya yi kamar shunayya;
yakan ɗauke hankalin sarki.
6 Kai! Ke kyakkyawa ce kuma kina sa ni jin daɗi,
Ya ƙaunatacciya, da farin cikin da kike kawo!
7 Tsayinki ya yi kamar itacen dabino,
kuma nonanki sun yi kamar 'ya'yan itace.
8 Na ce, "Zan hau itacen dabino;
zan kama 'ya'yansa."
Bari nonanki su zama kamar nonna kuringa,
ƙanshin numfashinki ya yi kamar gawasa,
9 kuma bakinki ya yi kamar ruwan inabi mafi kyau.

*Kaunatacciya*

Bari ruwan inabi yǎ wuce kai tsaye zuwa ga ƙaunataccena,
yana gudu a hankali a leɓuna da kuma haƙora.
10 Ni ta ƙaunataccena ce,
kuma sha'awarsa domina ne.
11 Ka zo, ƙaunataccena, bari mu je bayan gari,
bari mu kwana a ƙauye.
12 Bari mu tafi gonar inabi da sassafe
don mu ga ko kuringar ta yi 'ya'ya,
ko furanninsu sun buɗe,
ko rumman sun yi fure,
a can zan nuna maka ƙaunata.
13 Manta-uwa sun ba da ƙanshinsu,

* **6:12** Ko kuwa cikin keken yaƙin Amminadab; Ko kuwa cikin keken yaƙin mutanen sarki

a bakin ƙofa kuwa akwai kowane abinci mai daɗi,
sabo da tsoho,
da na ajiye dominka, ƙaunataccena.

# 8

1 Da a ce kai ɗan'uwa ne gare ni,
wanda nonon mahaifiyata sun shayar!
Da in na same ka a waje,
na sumbace ka,
babu wanda zai rena ni.
2 Da sai in bi da kai
in kawo ka gidan mahaifiyata,
ita da ta koyar da ni.
Da na ba ka ruwan inabi gaurayayye da kayan yaji ka sha,
zaƙin rumman nawa.
3 Hannunsa na hagu yana a ƙarƙashin kaina,
hannunsa na dama kuma ya rungume ni.
4 'Yan matan Urushalima, ku yi mini alkawari.
Ba za ku tā da ko ku farka ƙauna ba
sai haka ya zama lalle.

*Kawaye*

5 Wace ce wannan da take haurawa daga hamada
tana dogara a kan ƙaunataccenta?

*Kaunatacciya*

A ƙarƙashin itacen gawasa na farkar da ke,
a wurin da aka haife ki,
wurin da mahaifiyarki ta haife ki.
6 Ka sa ni kamar hatimi a zuciyarka,
kamar hatimi a hannunka;
gama ƙauna tana da ƙarfi kamar mutuwa,
kishinta yana kamar muguntar kabari,
yana ƙuna kamar wuta mai ci,
kamar gagarumar wuta.*
7 Ruwa da yawa ba zai iya kashe ƙauna ba,
koguna ba za su iya kwashe ta ba.
In wani zai bayar da
dukan dukiyar gidansa don ƙauna,
za a yi masa dariya ne kawai.

*Kawaye*

8 Muna da ƙanuwa,
nonanta ba su riga sun yi girma ba.
Me za mu yi da ƙanuwarmu
a ranar da za a yi maganar sonta?
9 Da a ce ita katanga ce,
da sai mu gina hasumiyar azurfa a kanta.
Da a ce ita ƙofa ce,
da sai mun yi mata ƙyauren itacen al'ul.

*Kaunatacciya*

10 Ni katanga ce
kuma nonaina sun yi kamar hasumiya.

---

* **8:6** Ko kuwa / kamar harshen wutar UBANGIJI.

Ta haka na zama idanunsa
kamar wanda yake kawo gamsuwa.
11 Solomon ya kasance da gonar inabi a Baʼal-Hamon;
ya ba da hayar gonar inabi ga ʼyan haya.
Kowanne zai biya shekel dubu na azurfa
don ʼyaʼyan inabin.
12 Amma gonar inabina nawa ne da zan bayar;
shekel dubu naka ne, ya Solomon,
kuma ɗari biyu na waɗanda suke lura da ʼyaʼyan itatuwansa ne.

*Kaunatacce*

13 Ke da kike zaune a cikin lambu
da ƙawaye suna lura da ke,
bari in ji muryarki!

*Kaunatacciya*

14 Ka zo, ƙaunataccena,
ka zama kamar barewa
ko kuwa kamar ʼyar batsiya
a kan dutsen da kayan yaji suke a shimfiɗe.

# Ishaya

1 Wahayi game da Yahuda da Urushalima wanda Ishaya ɗan Amoz ya gani a
zamanin da Uzziya, Yotam, Ahaz da Hezekiya, suka yi mulkin Yahuda.

### *Al'umma mai tayarwa*

2 Ku kasa kunne, ya sammai! Ki saurara, ya duniya!
Gama UBANGIJI ya yi magana,
"Na yi renon 'ya'ya, na kuma raya su,
amma sun tayar mini.
3 Saniya ta san maigidanta,
jaki ya san wurin sa wa dabbobi abinci maigidansa,
amma Isra'ila ba su sani,
mutanena ba su gane ba."

4 Kash, ya ke al'umma mai zunubi,
mutane cike da laifi,
tarin masu aikata mugunta,
'ya'yan da aka miƙa wa lalaci!
Sun yashe UBANGIJI;
sun rena Mai Tsarkin nan na Isra'ila
suka juya masa baya.

5 Me ya sa za a ƙara yin muku dūka?
Me ya sa kuka nace ga yin tayarwa?
An yi wa dukan kanku rauni,
zuciyarku duk tana ciwo.
6 Daga tafin ƙafarku zuwa saman kanku
ba lafiya,
sai miyaku da ƙujewa
da manyan gyambuna,
ba a tsabtacce su ba ko a daure
ko shafa musu magani.

7 Kasarku ta zama kufai,
an ƙone biranenku da wuta;
baƙi suna ƙwace gonakinku
a idanunku,
ta zama kango kamar sa'ad da baƙi suka rushe ta.
8 An bar diyar Sihiyona
kamar rumfar mai ƙumu a gonar inabi,
kamar bukka a gonar kabewa,
kamar birnin da aka kewaye da yaƙi.
9 Da ba a ce UBANGIJI Maɗaukaki
ya bar mana raguwar masu rai ba,
da mun zama kamar Sodom,
da mun zama kamar Gomorra.

10 Ku saurari maganar UBANGIJI,

ku masu mulkin Sodom;
ku kasa kunne ga dokar Allahnmu,
ku mutanen Gomorra!
11 UBANGIJI ya ce, “Yawan hadayunku,
mene ne suke a gare ni?”
Ina da isashen hadayun ƙonawa,
na raguna da na kitsen dabbobi masu ƙiba;
ba na jin daɗin
jinin bijimai da na tumaki da kuma na awaki.
12 Sa’ad da kuka zo don ku bayyana a gabana,
wa ya nemi wannan daga gare ku,
da kuke kai da kawowa a filayen gidana?
13 Ku daina kawo hadayu marasa amfani!
Turarenku abin ƙyama ne gare ni.
Ina ƙin bukukkuwanku na Sabon Wata, da na ranakun Asabbaci, da taronku na addini,
ba zan iya jure wa mugun taronku ba.
14 Bukukkuwanku na Sabon Wata da na tsarkakan ranaku
na ƙi su.
Sun zama mini kaya;
na gaji da ɗaukansu.
15 Sa’ad da kuka ɗaga hannuwanku wajen yin addu’a,
zan ɓoye fuskata daga gare ku;
ko da kun miƙa addu’o’i masu yawa,
ba zan kasa kunne ba.

Hannuwanku sun cika da jini!

16 Ku yi wanka ku kuma tsabtacce kanku.
Ku kawar da mugayen ayyukanku daga gabana;
Ku daina aikata mugunta.
17 Ku koyi yin nagarta; ku nemi adalci.
Ku ƙarfafa waɗanda aka zalunta.*
Ku ba wa marayu hakkinsu,
ku taimaki gwauruwa.

18 UBANGIJI ya ce,
“Yanzu fa ku zo, bari mu dubi batun nan tare,
Ko da zunubanku sun yi ja kamar garura,
za su zama fari kamar ƙanƙara;
ko da sun yi ja kamar mulufi,
za su zama kamar ulu.
19 In kuna da niyya kuna kuma yi mini biyayya,
za ku ci abubuwa masu kyau daga ƙasar;
20 amma in kuka yi tsayayya kuka kuma yi tayarwa,
za a kashe ku da takobi.”
Ni Ubangiji na faɗa.

21 Dubi yadda amintacciyar birni
ta zama karuwa!
Dā ta cika da yin gaskiya;

* **1:17** Ko kuwa / ku tsawata wa masu zalunci

dā masu adalci a can suke zama,
amma yanzu sai masu kisankai kaɗai!
22 Azurfarki ta zama jebu,
an gauraye ruwan inabinki mafi kyau da ruwa.
23 Masu mulkinki ʼyan tawaye ne,
abokan ɓarayi;
dukansu suna ƙaunar cin hanci
suna bin kyautai.
Ba sa taɓa tsare marayu a ɗakin shariʼa;
ba sa taimakon gwauruwa.

24 Saboda haka Ubangiji, UBANGIJI Maɗaukaki,
Mai Iko nan na Israʼila, ya furta,
“Kai, zan sami hutu daga maƙiyana
in kuma yi ramuwa a kan abokan gābana.
25 Zan juye hannuna a kanki;
zan wanke ke sarai
in fitar da dukan ƙazantarki.
26 Zan maido da alƙalanki kamar yadda suke a dā can,
mashawartanki kamar yadda suke da fari.
Bayan haka za a ce da ke
Birnin Masu Adalci,
Amintacciyar Birni.”

27 Za a fanshi Sihiyona da adalci,
masu tubanta kuma da aikin gaskiya.
28 Amma za a karye ʼyan tawaye da masu zunubi,
waɗanda suka rabu da UBANGIJI kuma za su hallaka.

29 “Za ku ji kunya saboda masujadan ƙarƙashin itatuwan oak
da kuka yi farin ciki;
za a kunyata ku saboda lambun
da kuka zaɓa.
30 Za ku zama kamar itacen oak mai busasshen ganyaye,
kamar lambu marar ruwa.
31 Mutum mai ƙarfi zai zama kamar rama,
aikinsa kuma kamar tartsatsin wuta;
duka za su ƙone tare,
ba kuwa wanda zai kashe wutar.”

# 2

*Dutsen UBANGIJI*

1 Ga abin da Ishaya ɗan Amoz ya gani game da Yahuda da Urushalima.

2 A kwanaki masu zuwa
za a kafa dutsen haikalin UBANGIJI
a matsayin babba cikin duwatsu;
za a daga shi bisa tuddai,
kuma dukan alʼummai za su bumbunto zuwa gare shi.
3 Mutane da yawa za su zo su ce,
“Ku zo, bari mu haura zuwa dutsen UBANGIJI,
zuwa gidan Allah na Yaƙub.

Zai koya mana hanyoyinsa,
domin mu yi tafiya cikin hanyoyinsa."
Dokar za tă fito daga Sihiyona,
maganar UBANGIJI daga Urushalima.
4 Zai shari'anta tsakanin al'ummai
zai kuma sulhunta faɗar mutane masu yawa.
Za su mai da takubansu su zama garemani
māsunsu su zama wuƙaƙen askin itatuwa.
Al'umma ba za tă ƙara ɗauki takobi a kan al'umma ba,
ba kuwa za su ƙara yin horarwar yaƙi.

5 Ki zo, ya gidan Yaƙub,
bari mu yi tafiya a hasken UBANGIJI.

*Ranar UBANGIJI*

6 Ka rabu da mutanenka,
gidan Yaƙub.
Sun cika da ayyukan sihiri da aka kawo daga Gabas;
suna yin duba kamar Filistiyawa
suna tafa hannuwa tare da marasa sanin Allah.
7 Kasarsu ta cika da azurfa da zinariya;
dukiyarsu kuma ba iyaka.
Kasarsu ta cika da dawakai;
kekunan yaƙinsu kuma ba iyaka.
8 Kasarsu ta cika da gumaka;
sukan rusuna ga aikin hannuwansu,
ga abin da yatsotsinsu suka yi.
9 Saboda an jawo mutum ƙasa
aka kuma ƙasƙantar da ɗan adam,
kada ku gafarta musu.*

10 Ku tafi cikin duwatsu,
ku ɓuya cikin ƙasa
daga razanar UBANGIJI
da kuma darajar ɗaukakarsa!
11 Za a ƙasƙantar da mai girman kai
za a kuma lalatar da fariyar masu ɗaga kai;
UBANGIJI kaɗai za a ɗaukaka a wannan rana.

12 UBANGIJI Maɗaukaki yana da rana ajiye
domin dukan masu girman kai da masu fariya
domin dukan waɗanda aka ɗaukaka
(zai kuwa ƙasƙantar da su),
13 domin dukan al'ul na Lebanon, masu tsayi da masu fariya,
da kuma dukan itatuwan oak na Bashan,
14 domin dukan dogayen duwatsu
da kuma tuddai masu tsayi,
15 domin kowace doguwar hasumiya
da kowace katanga mai ƙarfi,
16 domin kowane jirgin ruwan kasuwanci†

* **2:9** Ko kuwa kada a ɗaga su † **2:16** Da Ibraniyanci kowane jirgin ruwan Tarshish

da kuma jirgi mafi girma mafi kyau.
17 Za a jawo mai girman kai ƙasa
a kuma ƙasƙantar da mai ɗaga kai;
UBANGIJI kaɗai za a ɗaukaka a wannan rana,
18 za a kuma kawar da gumaka ƙaƙaf.

19 Mutane za su gudu zuwa kogwannin duwatsu
da kuma ramummuka a ƙasa
daga razanar UBANGIJI
da kuma darajar ɗaukakarsa,
sa'ad da ya tashi don yă girgiza duniya.
20 A wannan rana mutane za su zubar wa
jaba da jamage
gumakansu na azurfa da gumakansu na zinariya
da suka yi don su bauta musu.
21 Za su gudu zuwa kogwannin duwatsu
da kuma zuwa tsagaggun duwatsu
daga razanar UBANGIJI
da kuma darajar ɗaukakarsa,
sa'ad da ya tashi don yă girgiza duniya.

22 Ku daina dogara ga mutum,
wanda numfashi ne kawai yake da shi a hancinsa.
Wace daraja gare shi?

# 3

*Hukunci a kan Urushalima da Yahuda*

1 Yanzu ka duba fa, Ubangiji,
UBANGIJI Maɗaukaki,
yana shirin yă ɗauke kowane tanadi da taimako
daga Urushalima da Yahuda
dukan tanade-tanaden abinci da kuma dukan tanade-tanaden ruwa,
2 jarumi, da soja,
alƙali da annabi
masu duba da dattijo,
3 shugaban sojojin hamsin da mutum mai makami,
mai ba da shawara, gwanin sarrafa abubuwa da mai gwanintan dabo.

4 "Zan sa 'yan yara su zama shugabanninsu;
'yan yara kurum za su yi mulkinsu."

5 Mutane za su zalunci juna
mutum da mutum, maƙwabci da maƙwabci.
Yara za su rena tsofaffi,
ƙasƙantacce zai rena mai daraja.

6 Mutum zai kama ɗaya daga cikin 'yan'uwansa
a gidan mahaifinsa ya ce,
"Kana da abin sawa, ka zama shugabanmu;
wannan kango kuma yă zama a ƙarƙashinka!"
7 Amma a ranan nan zai tā da murya ya ce,

“Ba ni ɓa dai.
Ba ni da abinci ko abin sawa a gidana;
kada ka mai da ni shugaban mutane.”

8 Urushalima tana tangaɗi,
Yahuda yana fāɗuwa;
maganganunsu da ayyukansu suna gāba da UBANGIJI,
suna rena ɗaukakar kasancewarsa.
9 Fuskokinsu shaidu ne a kansu;
suna nuna zunubinsu a fili kamar yadda Sodom ya yi;
ba sa ma ɓoye shi.
Kaitonsu!
Sun jawo wa kansu masifa.

10 Ku faɗa wa masu adalci cewa kome zai zama musu da kyau,
gama za su ji daɗin aikin da hannuwansu suka yi.
11 Kaiton masu mugunta! Masifa tana a kansu!
Za a rama abin da hannuwansu suka yi.

12 Matasa suna zalunta mutanena,
mata suna mulki a bisansu.
Ya mutanena, jagorarinku suna ɓad da ku;
suna karkatar da ku daga hanya.

13 UBANGIJI ya ɗauki mazauninsa a cikin ɗakin shari’a;
ya tashi don yă shari’anta mutane.
14 UBANGIJI yana shari’a
da dattawa da kuma shugabannin mutanensa,
“Ku ne kuka lalace gonar inabina;
ganimar talakawa suna a gidajenku.
15 Ina dalilin da kuke marmatsa mutanena
kuna gurgurje fuskokin talakawa?”
Ni UBANGIJI Maɗaukaki na faɗa.

16 UBANGIJI ya ce,
“Matan Sihiyona suna da girman kai,
suna tafiya da wuya a miƙe,
da idanu masu yaudara,
suna takawa ɗaya-ɗaya a hankali,
da mundaye a ƙafafunsu, suna cas-cas.
17 Saboda haka Ubangiji zai kawo gyambuna a kawunan matan Sihiyona;
UBANGIJI zai sa a aske kawunansu, a bar su ƙwal.”
18 A wannan rana Ubangiji zai ƙwace abin da suke taƙama da shi, mundayensu,
ɗankwalin kansu da abin wuyansu, 19 ’yan kunnensu, kwandagansu da lulluɓinsu,
20 kitsonsu, sarƙar da suke sa wa damatsansu da ɗamararsu, kwalabai turare da layu,
21 da ƙawanen da suka sa a yatsotsinsu da hancinsu, 22 tufafi masu kyau, da manyan
rigunansu, da mayafansu, da jakar kuɗinsu 23 da madubi, da kuma tufafin lilin da
adikai, da gyale.
24 A maimakon ƙanshi, wari ne za a ji;
a maimakon abin ɗamara, igiya ce za a samu;
a maimakon kyakkyawan gashi, sanƙo za su kasance da shi a kai;

a maimakon tufafi masu kyau, za su sa tsummoki;
a maimakon kyau, za su zama munana.
25 Mazanku za su mutu ta wurin takobi,
jarumawanku za su mutu a yaƙi.
26 Kofofin Sihiyona za su yi makoki su kuma yi kuka;
za tă zama wofi, za tă zauna a ƙasa.

# 4

1 A wannan rana mata guda bakwai
za su cafke namiji guda
su ce, "Ma ciyar da kanmu
mu kuma yi wa kanmu sutura;
ka dai bari mu ce kai ne mijinmu.
Ka ɗauke mana kunyar da za mu sha."

*Reshen UBANGIJI*

2 A wannan rana Reshen UBANGIJI zai zama kyakkyawa da kuma ɗaukaka, kuma
amfanin ƙasar zai zama abin fariya da ɗaukakar waɗanda suka rayu a Isra'ila.
3 Waɗanda suka rage a Sihiyona, waɗanda suka rage a Urushalima, za a ce da su masu
tsarki, wato, dukan waɗanda aka rubuta a cikin masu rai a Urushalima. 4 Ubangiji
zai wanke duk wani ƙazantar matan Sihiyona; ya tsabtacce jinin da aka zubar daga
Urushalima ta wurin ruhun hukunci da yake ƙuna kamar wuta. 5 Sa'an nan UBANGIJI
zai sa girgijen hayaƙi da rana da harshen wuta da dare a bisa dukan Dutsen Sihiyona
da kuma bisa waɗanda suka tattaru a can; a bisa duka kuwa ɗaukakar za tă zama
rumfa. 6 Za tă zama rumfa da inuwar da za tă tare zafin rana, da kuma mafaka da
wurin ɓuya daga hadari da ruwan sama.

# 5

*Waƙar gonar inabi*

1 Zan rera waƙa wa ƙaunataccena
waƙa game da gonar inabinsa.
Kaunataccena yana da gonar inabi
a gefen tudu mai dausayi.
2 Ya haƙa ƙasa ya kuma tsintsince duwatsun
ya shuka mata inabi mafi kyau.
Ya gina hasumiyar tsaro a cikinta
ya kuma shirya wurin matsin ruwan inabi.
Sa'an nan ya sa rai ga samun girbi mai kyau na inabin,
amma sai ga shi inabin ya ba da munanan 'ya'ya.

3 "Yanzu fa ku mazauna cikin Urushalima da mutanen Yahuda,
ku shari'anta tsakanina da gonar inabina.
4 Me kuma ya rage da za a yi wa gonar inabina
fiye da abin da na yi mata?
Da na nemi inabi masu kyau,
me ya sa ta ba da munana 'ya'ya?
5 Yanzu zan faɗa muku
abin da zan yi da gonar inabina.
Zan cire katangar da ta kewaye ta,
za tă kuwa lalace;
zan rushe bangonta,

za a kuwa tattake ta.
6 Zan mai da ita kango,
ba zan aske ta ba, ba kuwa zan nome ta ba,
sarƙaƙƙiya da ƙayayyuwa kuwa za su yi girma a can
Zan umarci gizagizai
kada su yi ruwan sama a kanta."

7 Gonar inabin UBANGIJI Maɗaukaki
ita ce gidan Isra'ila,
mutanen Yahuda kuma
su ne lambun farin cikinsa.
Yana kuma nema ganin gaskiya, amma sai ga zub da jini;
yana neman adalci, amma sai ga shi kukan azaba yake ji.

*Kaito da hukunce-hukunce*

8 Kaitonku ku waɗanda kuke ƙara wa kanku gidaje
kuke kuma haɗa gonaki da gonaki
har babu sauran filin da ya rage
ku kuma zauna ku kaɗai a ƙasar.
9 UBANGIJI Maɗaukaki ya furta a kunnuwana,
"Tabbatacce manyan gidajen za su zama kango,
za a bar kyawawan gidajen nan ba kowa.
10 Kadada goma na gonar inabi zai ba da garwan ruwan inabi ɗaya kaɗai,
mudu guda na iri kuma zai ba da efa na hatsi guda kurum."

11 Kaiton waɗanda suke tashi da sassafe
don su nufi wurin shaye-shaye,
waɗanda suke raba dare
har sai sun bugu da ruwan inabi.
12 Suna kaɗa garaya, da molaye a bukukkuwansu,
ganguna da busa da ruwan inabi,
amma ba su kula da ayyukan UBANGIJI ba,
ba sa biyayya ga aikin hannuwansa.
13 Saboda haka mutanena za su yi zaman bauta
domin rashin fahimi;
manyan mutanensu za su mutu da yunwa
talakawansu kuma su mutu da ƙishirwa.
14 Saboda haka kabari ya fadada marmarinsa
ya kuma buɗe bakinsa babu iyaka;
cikinsa manyan mutanensu da talakawansu za su gangara
tare da dukan masu hayaniyarsu da masu murnansu.
15 Ta haka za a ƙasƙantar da mutum
kuma za a ƙasƙantar da 'yan adam,
za a ƙasƙanta da masu girman kai.
16 Amma UBANGIJI Maɗaukaki zai sami ɗaukaka ta wurin aikata gaskiya,
kuma Allah mai tsarki zai nuna kansa ta wurin adalcinsa.
17 Sa'an nan tumaki za su yi kiwo kamar yadda suke yi a wurin kiwonsu;
raguna za su yi kiwo cikin abubuwa masu kyau da suka lalace.

18 Kaiton waɗanda suke jan zunubi da igiyar ruɗu,
da kuma mugunta da igiyoyin keken yaƙin,
19 waɗanda suke cewa, "Bari Allah yǎ gaggauta,
bari yǎ hanzarta aikinsa

don mu gani.
Bari yă iso,
bari shirin Mai Tsarkin nan na Isra'ila yă zo,
don mu sani."

20 Kaiton waɗanda suke ce da mugunta nagarta
nagarta kuma mugunta,
waɗanda suke mai da duhu haske
haske kuma duhu,
waɗanda suke mai da ɗaci zaƙi
zaƙi kuma ɗaci.

21 Kaiton waɗanda suke tsammani suna da hikima
da kuma wayo a idonsu.

22 Kaiton waɗanda suke jarumawa a shan ruwan inabi
da gwanaye a haɗin abubuwan sha,
23 waɗanda suke ƙyale masu laifi don sun ba da cin hanci,
amma su hana a yi gaskiya wa marasa laifi.
24 Saboda haka kamar yadda harshen wuta yakan lashe kara
kuma kamar yadda busasshiyar ciyawa takan ƙone ƙurmus a cikin wuta,
haka saiwarsu za su ruɓa
iska kuma ta hura furanninsu kamar ƙura;
gama sun ƙi dokar UBANGIJI Maɗaukaki
suka kuma ƙyale maganar Mai Tsarkin nan na Isra'ila.
25 Saboda haka fushin UBANGIJI ya yi ƙuna a kan mutanensa;
ya ɗaga hannunsa ya kuma buge su.
Duwatsu sun jijjigu,
gawawwaki kuwa suka zama kamar juji a tituna.

Saboda wannan duka, fushinsa bai huce ba,
bai kuwa janye hannunsa ba.

26 Ya ɗaga tuta don al'ummai masu nisa,
ya yi feɗuwa wa waɗanda suke a iyakar duniya.
Ga shi sun iso,
da sauri da kuma gaggawa!
27 Babu ko ɗayansu da ya gaji ko ya yi tuntuɓe,
babu ko ɗaya da ya yi gyangyaɗi ko barci;
babu abin ɗamarar da ya kunce a gindi,
ba igiyar takalmin da ta tsinke.
28 Kibiyoyinsu masu tsini ne,
an ɗaura dukan bakkunansu;
kofatan dawakansu sun yi kamar dutsen ƙanƙara,
ƙafafun keken yaƙinsu kamar guguwa ne.
29 Rurinsu ya yi kamar na zaki,
suna ruri kamar 'yan zakoki;
suna yin gurnani yayinda suke kamun abin da suke farauta
su ɗauke shi ba mai ƙwace shi.
30 A wannan rana za su yi ta ruri a kansa
kamar rurin teku.
Kuma in wani ya dubi ƙasar,

zai ga duhu da damuwa;
haske ma zai zama duhu ta wurin gizagizai.

# 6

*Aikin Ishaya*

1 A shekarar da Sarki Uzziya ya mutu, na ga Ubangiji zaune a kan kujerar sarauta
a sama cike da ɗaukaka, zatinsa ya cika haikali. 2 A bisansa akwai serafofi, kowanne
yana da fikafikai shida. Fikafikai biyu sun rufe fuskokinsu, da biyu suka rufe
ƙafafunsu, biyu kuma da su suke tashi. 3 Suna kiran juna,

“Mai Tsarki, Mai Tsarki, Mai Tsarki! UBANGIJI Maɗaukaki ne;
duniya ta cika da ɗaukakarsa.”

4 Da jin ƙarar muryoyinsu madogarai da madogaran ƙofa suka girgiza, haikali kuma
ya cika da hayaƙi.

5 Sai na tā da murya na ce, “Kaitona! Na shiga uku! Gama ni mutum ne mai leɓuna
marar tsarki, kuma ina raye a cikin mutane masu leɓuna marasa tsarki, idanuna
kuma sun ga Sarki, UBANGIJI Maɗaukaki.”

6 Sai ɗaya daga cikin serafofin ya yi firiya zuwa wurina tare da garwashi mai wuta
a hannunsa, wanda ya ɗiba da arautaki daga bagade. 7 Da shi ne ya taɓa bakina ya
ce, “Duba, wannan ya taɓa leɓunanka, yanzu fa an kawar da laifofinka, an kuma
gafarta maka zunubanka.”

8 Sa’an nan na ji muryar Ubangiji tana cewa, “Wa zan aika? Wa zai tafi mana?”

Sai na ce, “Ga ni! Ka aike ni!”

9 Ya ce, “Je ka ka faɗa wa wannan mutane,

“ ‘Kome yawan kasa kunne da za ku yi, ba za ku fahimta ba;
Kome yawan dubar da za ku yi, ba za ku san abin da yake faruwa ba.’

10 Ka sa zuciyar mutanen nan ta dushe;
kunnuwansu su kurunce,
idanunsu kuma su makance.
In ba haka ba za su iya gani da idanunsu,
su ji da kunnuwansu,
su fahimta da zuciyarsu,
su kuma juyo a kuma warkar da su.”

11 Sa’an nan na ce, “Har yaushe, ya Ubangiji?”

Ya kuma amsa,

“Sai an lalatar da biranen
ba kowa a ciki,
sai an mai da gidaje kangwaye
ƙasa kuma ta zama kango ba amfani,
12 sai lokacin da Ubangiji ya kori kowa
aka kuma yashe ƙasar gaba ɗaya.
13 Ko da yake kashi ɗaya bisa goma zai ragu a ƙasar,
za tă sāke zama kango.
Amma kamar yadda katambiri da itacen oak
sukan bar kututturai sa’ad da aka yanke su,
haka iri mai tsarkin nan zai zama kututture a ƙasar mai tsarki.”

# 7

*Alamar Immanuwel*

1 Sa'ad da Ahaz ɗan Yotam, ɗan Uzziya, yake sarkin Yahuda, Sarki Rezin na Aram
da Feka ɗan Remaliya sarkin Isra'ila suka haura don su yaƙi Urushalima, amma ba
su iya cinta da yaƙi ba.

2 Sai fa aka faɗa wa gidan Dawuda cewa, "Aram ya haɗa kansa* da Efraim"; saboda
haka zuciyar Ahaz da ta mutanensa suka firgita, sai ka ce itatuwa a kurmin da iska
ta girgiza.

3 Sai Ubangiji ya ce wa Ishaya, "Fita, kai da ɗanka Sheyar-Yashub,† don ku sadu da
Ahaz a ƙarshen wuriyar da take kawo ruwa daga Tafkin Tudu, a hanyar Filin Mai
Wanki. 4 Ka faɗa masa, 'Ka yi hankali, ka natsu kada kuma ka ji tsoro ko ka damu,
kada ka ji tsoron fushin sarki Rezin da na Aram da na ɗan Remaliya, ba wani abu mai
hatsari ba ne, bai fi hayaƙin 'yan ƙirare biyu da suke cin wuta ba. 5 Aram, Efraim da
ɗan Remaliya sun ƙulla maƙarƙashiya, suna cewa, 6 "Bari mu kai wa Yahuda hari;
bari mu yayyage su mu rarraba su a tsakaninmu, mu naɗa Tabeyel sarki a kansu."
7 Duk da haka ga abin da Ubangiji Mai Iko Duka ya ce,

" 'Ba zai faru ba,
ba zai auku ba,
8 gama kan Aram shi ne Damaskus,
kan Damaskus kuma kawai shi ne Rezin.
Cikin shekaru sittin da biyar
za a wargaje Efraim har ba za tă iya rayuwa ta zama al'umma ba.
9 Kan Efraim shi ne Samariya,
kan Samariya kuma kawai shi ne ɗan Remaliya.
In ba ku tsaya da ƙarfi cikin bangaskiyarku ba,
ba za ku dawwama ba.' "

10 Ubangiji ya kuma yi magana wa Ahaz ya ce, 11 "Ka roƙi Ubangiji Allahnka yă ba
ka alama, ko daga zurfafa masu zurfi ko kuwa daga can cikin sama."

12 Amma Ahaz ya ce, "Ba zan nema ba; ba zan gwada Ubangiji ba."

13 Sa'an nan Ishaya ya ce, "To, ku saurara, ya ku gidan Dawuda! Abin kirki kuke
yi ne da kuka ƙure haƙurin jama'a? Ko haƙurin Allah ne kuma kuke so ku ƙure?
14 Saboda haka Ubangiji kansa zai ba ku alama. Ga shi budurwa za tă yi ciki, za tă haifi
ɗa, za tă kuwa kira shi Immanuwel. 15 In ya yi girma har ya isa yanke shawara don
kansa, madara da zuma ne abincinsa. 16 Amma kafin yaron yă isa yanke shawara
yă ƙi abin da yake mummuna, yă zaɓi abin da yake nagari, ƙasashen sarakunan
nan biyu da kuke tsoro za su zama kango. 17 Ubangiji zai aukar maka da kwanakin
wahala, kai da jama'arka, da dukan iyalin gidan sarauta, waɗanda suka fi muni tun
lokacin da aka raba mulkin Efraim daga na Yahuda, zai kawo sarkin Assuriya."

18 A wannan rana Ubangiji zai yi feɗuwa yă kira ƙudaje daga rafuffuka masu
nisa na Masar da kuma ƙudan zuma daga ƙasar Assuriya. 19 Za su zo su mamaye
kwazazzabai da kogwanni cikin duwatsu, a kan dukan ƙayayyuwa da dukan
rammukan ruwa.

20 A wannan rana Ubangiji zai yi amfani da rezan da aka yi haya daga ƙetaren
Kogi,‡ sarkin Assuriya ke nan, yă aske kanku da gashin ƙafafunku, zai kuma aske
gemunku. 21 A ranar, mutum zai bar karsana ɗaya da awaki biyu da rai. 22 Kuma
saboda yalwa madarar da suke bayarwa, zai kasance da madarar da zai sha. Dukan
waɗanda suka rage a ƙasar za su sha madara da zuma. 23 A wannan rana, a kowane
wuri inda akwai kuringa dubu da kuɗinsu ya kai shekel dubu na azurfa, ƙayayyuwa
da sarƙaƙƙiya ne kawai za su kasance a can. 24 Mutane za su je can da baka da
kibiyoyi, gama ƙayayyuwa da sarƙaƙƙiya ne za su rufe ƙasar. 25 Game da dukan
tuddai da dā ake nome da garemani kuwa, ba za ku ƙara je wurin ba saboda tsoron

* 7:2 Ko kuwa ya kafa sansani a † 7:3 Sheyar-Yashub yana nufin raguwa za tă komo. ‡ 7:20 Wato, Yuferites.

ƙayayyuwa da sarƙaƙƙiya; za su zama wuraren da ake kai shanu a sake su su yi ta yawo da kansu, tumaki kuma su yi ta gudu.

# 8

## *Assuriya kayan aikin* UBANGIJI

1 UBANGIJI ya ce mini, "Ka ɗauki naɗaɗɗen littafi mai girma ka yi rubutu a kai da
alƙalami kurum, Maher-Shalal-Hash-Baz.* 2 Zan kuma kira Uriya firist da Zakariya
ɗan Yeberekiya su zama mini amintattun shaidu."
3 Sa'an nan na tafi na yi jima'i da annabiya, ta kuwa yi ciki ta haifi ɗa. UBANGIJI
kuma ya ce mini, "Raɗa masa suna, Maher-Shalal-Hash-Baz. 4 Kafin yaron yă san
yadda zai ce 'Babana' ko 'Mamana,' sarkin Assuriya zai kwashe arzikin Damaskus
da ganimar Samariya."
5 UBANGIJI ya sāke yi mini magana ya ce,
6 "Domin wannan jama'a ta ƙi
natsattsen ruwan rafin Shilowa
suka yi ta farin ciki a kan Rezin
ɗan Remaliya,
7 saboda haka Ubangiji yana shirin yă kawo musu
rigyawar ruwan Kogi,†
wato, sarkin Assuriya da dukan sojojinsa.
Zai cika dukan gaɓoɓinsa,
yă kuma malala har zuwa bakin kogi.
8 Yă yi ta malala har zuwa cikin Yahuda, yă shafe ta,
yana ratsa ta ciki har yă kai kafaɗa.
Fikafikansa da ya buɗe za su rufe fāɗin ƙasarka,
Ya Immanuwel!"‡

9 Ku yi kururuwar yaƙi, ku ƙasashe, ku kuma ji tsoro!
Ku saurara, dukanku manisantan ƙasashe.
Ku shirya don yaƙi, ku kuma ji tsoro!
10 Ku ƙirƙiro dabarunku, amma ba za su yi nasara ba;
ku ƙulla shirye-shiryenku, amma ba za su yi amfani ba,
gama Allah yana tare da mu.§

## *Ji tsoron Allah*

11 UBANGIJI ya yi mini magana da hannunsa mai ƙarfi a kaina, yana yi mini gargaɗi
kada in bi hanyar waɗannan mutane. Ya ce,
12 "Kada ka kira wani abu makirci
game da kome da waɗannan mutane suke kira makirci;*
kada ji tsoron abin da suke tsoro,
kada kuma ka firgita game da shi.
13 UBANGIJI Maɗaukaki shi ne za ka ɗauka a matsayi mai tsarki,
shi ne wanda za ka ji tsoro,
shi ne za ka yi rawar jiki a gabansa,
14 zai kuwa kasance a wuri mai tsarki;
amma ga dukan gidajen Isra'ila zai zama
dutsen da zai sa mutane su yi tuntuɓe

* **8:1** Maher-Shalal-Hash-Baz yana nufin kwashe ganima nan da nan, washe kayan da aka ci a yaƙi da hanzari; haka ma a 3. † **8:7** Wato, Yuferites. ‡ **8:8** Immanuwel yana nufin Allah tare da mu. § **8:10** Da Ibraniyanci Immanuwel * **8:12** Ko kuwa Kada ka ce a yi yarjejjeniya a kowane lokacin da mutanen nan suka ce a yi yarjejjeniya

dutse kuma da zai sa su fāɗi.
Ga dukan mutanen Urushalima kuma zai zama
tarko da raga.
15 Yawancinsu za su yi tuntuɓe;
za su fāɗi a kuwa ragargaza su,
za a sa musu tarko a kuma kama su."

16 Ɗaura shaidar nan ta gargadi
ka kuma yimƙe umarnin Allah a cikin almajiraina.
17 Zan saurari Ubangiji,
wanda ya ɓoye fuskarsa daga gidan Yaƙub.
Zan dogara gare shi.
18 Ga ni, da yaran da Ubangiji ya ba ni. Mu alamu ne da shaidu a cikin Isra'ila daga
Ubangiji Maɗaukaki, wanda yake zama a Dutsen Sihiyona.
19 Sa'ad da mutane suka ce muku ku nemi shawarar 'yan bori da masu sihiri,
waɗanda suke shaƙe murya har ba a jin abin da suke faɗi, bai kamata mutane su
nemi shawara daga Allahnsu ba? Me zai sa ku nemi shawara daga matattu a madadin
masu rai? 20 Nemi umarnin Allah da kuma shaidar jan kunne. Duk wanda bai yi
magana bisa ga wannan kalma ba, ba su da amfani. 21 Cikin matsuwa da yunwa, za
su yi ta kai komo ko'ina a ƙasar; sa'ad da suka ji yunwa, za su yi fushi su tā da idanu
sama, su zagi sarkinsu da Allahnsu. 22 Sa'an nan za su zura wa ƙasa idanu, abin da
za su gani kawai shi ne matsuwa da duhu da kuma abin banrazana, za a kuma jefa
su cikin baƙin duhu.

# 9

*A gare mu an haifi yaro*

1 Duk da haka, babu sauran baƙin ciki ga waɗanda suke shan azaba. Dā ya
ƙasƙantar da ƙasar kabilan Zebulun da ƙasar Naftali, amma nan gaba zai girmama
Galili na Al'ummai, ta hanyar teku wadda take ta Urdun.
2 Mutanen da suke tafiya cikin duhu
sun ga babban haske;
a kan waɗanda suke zama a ƙasar inuwar mutuwa*
haske ya haskaka.
3 Ka fadada al'umma
ka kuma ƙara farin cikinsu;
suna farin ciki a gabanka
yadda mutane sukan yi murna a lokacin girbi,
kamar yadda mutane sukan yi farin ciki
sa'ad da suke raba ganima.
4 Gama kamar yadda yake a kwanakin da aka ci Midiyan da yaƙi,
kuka ji tsoro
nauyin da ya nawaita musu,
sandar da yake a kafaɗunsu,
sandar masu zaluncinsu.
5 Kowane takalmin jarumin da aka yi amfani da shi a yaƙi
da kuma kowane rigar da ka naɗe cikin jini
zai kasance an ƙone shi
zai kuma zama abin hura wuta.
6 Gama a gare mu an haifa mana yaro,
a gare mu an ba da ɗa,

* **9:2** Ko kuwa ƙasar duhu

gwamnati za tă kasance a kafaɗarsa.
Za a ce da shi
Mashawarci Mai Banmamaki, Allah Maɗaukaki
Uban Madawwami, Sarkin Salama.
7 Game da girmar gwamnatinsa da salama
babu iyaka.
Zai gāji sarki Dawuda, yă yi mulki a matsayinsa,
zai kafa mulkinsa a kan adalci da gaskiya,
tun daga yanzu har zuwa ƙarshen zamani.
UBANGIJI Maɗaukaki ne
ya yi niyyar aikata wannan duka.

### *Fushin UBANGIJI a kan Isra'ila*

8 Ubangiji ya aika da saƙon gāba da Yaƙub;
zai auka wa Isra'ila.
9 Dukan mutane za su san shi,
Efraim da mazaunan Samariya,
waɗanda suke magana da fariya
suna kuma ɗaga kai,
10 "Tubalai sun zube a ƙasa,
amma za mu sāke gina su da dutse;
an sassare itatuwan ɓaure,
amma za mu maya su da al'ul."
11 Amma UBANGIJI ya ƙarfafa maƙiyan Rezin gāba da su
ya kuma ingiza abokan gāba.
12 Arameyawa daga gabas da Filistiyawa daga yamma
sun cinye Isra'ila da buɗaɗɗen baki.

Duk da haka, fushinsa bai huce ba,
hannunsa har yanzu yana a miƙe.

13 Amma mutanen ba su juyo wurin wanda ya buge su ba,
balle su nemi UBANGIJI Maɗaukaki.
14 Saboda haka UBANGIJI zai yanke Isra'ila kai da wutsiya,
da reshen dabino da iwa a rana guda;
15 dattawa da manyan mutane su ne kai,
annabawa waɗanda suke koyar da ƙarairayi su ne wutsiya.
16 Waɗanda suke jagorar wannan mutane suna ɓad da su,
su ne waɗanda ake jagora aka sa suka kauce.
17 Saboda haka Ubangiji ba zai ji daɗin matasa ba,
ba kuwa zai ji tausayin marayu da gwauraye ba,
gama kowa marar sanin Allah ne da kuma mugu,
kowane baki yana faɗin mugayen maganganu.

Duk da haka, fushinsa bai huce ba,
hannunsa har yanzu yana a miƙe.

18 Tabbatacce mugunta tana ƙuna kamar wuta;
tana cin ƙayayyuwa da sarƙaƙƙiya,
ta sa wuta a jeji mai itatuwa masu yawa,
don yă yi murtuke hayaƙi har zuwa sama.
19 Ta wurin fushin UBANGIJI Maɗaukaki

ƙasar za tă ci wuta
mutane kuma za su zama abin hura wutar,
babu wanda zai ji tausayin ɗan'uwansa.
20 A dama za su ci,
amma su ci gaba da jin yunwa;
a hagu za su ci,
amma ba za su ƙoshi ba.
Kowa zai mai da naman 'ya'yansa abinci.
21 Manasse zai mai da Efraim abinci, Efraim kuma yă cinye Manasse;
tare za su yi gāba da Yahuda.

Duk da haka, fushinsa bai huce ba,
hannunsa har yanzu yana a miƙe.

# 10

1 Kaiton waɗanda suke kafa dokokin rashin gaskiya,
waɗanda suke ba da ƙa'idodin danniya,
2 don su hana matalauta hakkinsu
su kuma ƙi yin shari'ar gaskiya a kan waɗanda suke zaluntar mutanena,
suna ƙwace wa gwauraye dukiyarsu
suna kuma yi wa marayu ƙwace.
3 Me za ku yi a ranan nan ta hukunci,
sa'ad da masifa ta zo daga nesa?
Ga wa za ku tafi don neman taimako?
Ina za ku bar dukiyarku?
4 Babu abin da zai rage sai cizon haƙora a cikin kamammu
ko mutuwa cikin waɗanda aka kashe.

Duk da haka, fushinsa bai huce ba,
hannunsa har yanzu yana a miƙe.

### *Hukuncin Allah a kan Assuriya*

5 "Kaiton Assuriya, sandar fushina,
a hannun da kulkin fushina yake!
6 Na aike shi gāba da al'umma marar sanin Allah,
na tura shi gāba da mutanen da suka ba ni fushi,
don yă kwashe ganima yă kuma yi wason ganima,
yă tattake su kamar laka a tituna.
7 Amma ba abin da ya yi niyya ke nan ba,
ba abin da yake da shi a zuciya ba;
manufarsa shi ne yă hallaka,
yă kuma kawo ƙarshen al'ummai da yawa.
8 Ya ce, 'Dukan shugabannin yaƙina ba sarakuna ba ne?'
9 'Kalno bai kasance kamar Karkemish ba?
Hamat bai zama kamar Arfad
Samariya kuma kamar Damaskus ba?
10 Yadda hannuna ya ƙwace mulkokin gumaka,
mulkokin da siffofinsu suka fi na Urushalima da Samariya,
11 ba zan yi da Urushalima da siffofinta
yadda na yi da Samariya da gumakanta ba?' "

12 Sa'ad da Ubangiji ya gama dukan aikinsa gāba da Dutsen Sihiyona da Urushalima,
zai ce, "Zan hukunta sarkin Assuriya saboda fariya na gangancin zuciyarsa da kuma
kallon reni na idanunsa. 13 Gama ya ce,
" 'Ta wurin ƙarfin hannuna ne na aikata wannan,
da kuma ta wurin hikimata, gama ina da fahimi.
Na kau da iyakokin ƙasashe,
na washe dukiyarsu;
a matsayina na mai iko, na mamaye sarakunansu.
14 Kamar yadda mutum yakan miƙa hannu cikin sheƙar tsuntsu
haka hannuna ya je ya washe dukiyar al'ummai;
kamar yadda mutane sukan tattara ƙwai,
haka na tattara dukan ƙasashe;
ba tsuntsun da ya kakkaɓe fikafiki,
ko yă buɗe baki don yă yi kuka.' "

15 Gatari ya taɓa fin wanda yake amfani da shi girma,
ko zarto yă yi wa wanda yake amfani da shi taƙama?
Sanda za tă girgiza mutumin da yake riƙe da ita,
ko kuwa kulki yă jijjiga mutumin da yake riƙe da katako!
16 Saboda haka UBANGIJI Maɗaukaki,
zai aukar da cuta mai kisa a kan ƙosassu jarumawa;
a ƙarƙashin sansaninsa zai ƙuna wuta
kamar harshen wuta.
17 Hasken Isra'ila zai zo kamar wuta,
Mai Tsarkinsu zai zama kamar wuta;
a rana guda zai ƙone yă kuma cinye
ƙayayyuwa da sarƙaƙƙiyarsa.
18 Darajar jejinsa da gonakinsa masu dausayi
za a hallaka su ɗungum,
kamar yadda ciwo yakan kashe mutum.
19 Sauran itatuwan jejinsa kuma za su ragu
ko ɗan ƙaramin yaro ma zai iya ƙidaya su.

### *Raguwar Isra'ila*

20 A wannan rana raguwar Isra'ila,
waɗanda suka ragu na gidan Yaƙub,
ba za su ƙara dogara ga
wanda ya kusa hallaka su ba
amma za su dogara ga UBANGIJI,
Mai Tsarkin nan na Isra'ila.
21 Raguwa za tă komo,* raguwar Yaƙub
za su komo ga Maɗaukaki Allah.
22 Ko da yake mutanenka, ya Isra'ila, sun zama kamar yashin bakin teku,
raguwa ce kurum za tă komo.
A ƙaddara hallaka,
mai mamayewa da mai adalci.
23 UBANGIJI Maɗaukaki, zai sa
hallakar da aka ƙaddara a kan dukan ƙasa ta faru.
24 Saboda haka, ga abin da UBANGIJI Maɗaukaki ya ce,
"Ya mutanena masu zama a Sihiyona,

* **10:21** Da Ibraniyanci sheyar-yashub; haka ma a aya 22.

kada ku ji tsoron Assuriyawa,
waɗanda suka dūke ku da sanda
suka kuma ɗaga kulki a kanku, kamar yadda Masar ta yi.
25 Ba da daɗewa ba fushina a kanku zai zo ga ƙarshe
hasalata kuma za tă koma ga hallakarsu."

26 UBANGIJI Maɗaukaki zai bulale su da tsumagiya,
kamar sa'ad da ya bugi Midiyan a dutsen Oreb;
zai kuma ɗaga sandarsa a bisa ruwaye,
yadda ya yi a Masar.
27 A wannan rana zai ɗauke nauyi daga kafaɗarku,
nauyinsu daga wuyanku;
za a karye karkiya
domin kun yi ƙiba ƙwarai.

28 Sun shiga Ayiyat;
sun bi ta Migron;
sun adana tanade-tanade a Mikmash.
29 Suka ƙetare ta hanya, suka kuma ce,
"Za mu kwana a Geba."
Rama ta firgita;
Gibeya ta Shawulu ta gudu.
30 Ki yi ihu, ya Diyar Gallim!
Ki saurara, ya Layisha!
Kayya, Anatot abin tausayi!
31 Madmena tana gudu;
mutanen Gebim sun ɓuya.
32 A wannan rana za su dakata a Nob;
za su jijjiga ƙarfinsu
a dutsen Diyar Sihiyona,
a tudun Urushalima.

33 Duba, UBANGIJI Maɗaukaki,
zai ragargaza rassa da iko mai girma.
Za a sassare itatuwa masu ganyaye,
za a yanke dogayen itatuwa har ƙasa.
34 Zai sassare itatuwan jeji da gatari har ƙasa;
Lebanon zai fāɗi a gaban Mai Iko.

# 11

*Reshe daga Yesse*

1 Toho zai fito daga kututturen Yesse;
daga saiwarsa Reshe zai ba da 'ya'ya.
2 Ruhun UBANGIJI zai kasance a kansa,
Ruhun hikima da na fahimta,
Ruhun shawara da na iko,
Ruhun sani da na tsoron UBANGIJI,
3 zai kuwa ji daɗin tsoron UBANGIJI.

Ba zai yi hukunci ta wurin abin da ya gani da idanunsa ba,
ba zai kuwa yanke shawara ta wurin abin da ya ji da kunnuwansa ba;

4 amma da adalci zai yi wa masu bukata shari'a,
da gaskiya zai yanke shawarwari saboda matalautan duniya.
Kamar sanda zai bugi duniya da maganar bakinsa;
da numfashin leɓunansa zai yanke mugaye.
5 Adalci ne zai zama abin ɗamararsa
aminci kuma igiyar da zai ɗaura kewaye da gindinsa.

6 Kyarkeci zai zauna tare da ɗan rago
damisa za tă kwanta tare da akuya,
ɗan maraƙi da zaki da ɗan saniya za su yi kiwo tare;
ɗan yaro ne zai lura da su.
7 Saniya da beyar za su yi kiwo tare,
ƙananansu za su kwanta tare,
zaki kuma zai ci ciyawa kamar saniya.
8 Jariri zai yi wasa kurkusa da ramin gamsheƙa,
ɗan yaro kuma zai sa hannunsa a ramin maciji mai mugun dafi.
9 Ba za su yi lahani ko su hallaka
wani a dutsena mai tsarki ba,
gama duniya za tă cika da sanin UBANGIJI
kamar yadda ruwaye suka rufe teku.

10 A wannan rana Saiwar Yesse zai miƙe kamar tuta don mutanenta; al'ummai za
su tattaru wurinsa, wurin hutunsa kuma zai zama mai daraja. 11 A wannan rana
Ubangiji zai miƙa hannunsa sau na biyu don yă maido da raguwar da ta rage na
mutanensa daga Assuriya, daga Masar ta Kasa, daga Masar ta Bisa,[*] daga Kush,[†]
daga Elam, daga Babiloniya,[‡] daga Hamat da kuma daga tsibiran teku.
12 Zai tā da tuta saboda al'ummai
yă kuma tattara masu zaman bauta na Isra'ila;
zai tattara mutanen Yahuda da suke a warwatse
kusurwoyi huɗu na duniya.
13 Kishin Efraim zai ɓace,
za a kuma kau da abokan gāban Yahuda;
Efraim ba zai yi kishin Yahuda ba,
haka ma Yahuda ba zai yi gāba da Efraim ba.
14 Tare za su fāɗa wa Filistiyawa da yaƙi daga yamma;
tare za su washe mutane wajen gabas.
Za su ɗibiya hannuwa a kan Edom da Mowab,
Ammonawa kuma za su yi musu biyayya.
15 UBANGIJI zai busar da
bakin tekun Masar;
da iska mai zafi zai share hannunsa
a bisa Kogin Yuferites[§]
Zai rarraba shi yă zama ƙanana rafuffuka bakwai
saboda mutane su iya hayewa da ƙafa.
16 Za a yi babbar hanya saboda raguwa mutanensa
da ta rage daga Assuriya,
kamar yadda ta kasance wa Isra'ila
sa'ad da suka fito daga Masar.

---

* **11:11** Da Ibraniyanci daga Faturos † **11:11** Wato, yankin Nilu na Bisa ‡ **11:11** Da Ibraniyanci Shinar
§ **11:15** Da Ibraniyanci Kogi

# 12

*Waƙoƙin yabo*

1 A wannan rana za ku ce,
“Zan yabe ka, ya UBANGIJI.
Ko da yake a dā ka yi fushi da ni,
amma yanzu ka daina fushi da ni
ka kuwa ta’azantar da ni.
2 Tabbatacce Allah shi ne mai cetona;
zan dogara gare shi ba kuwa zan ji tsoro ba.
UBANGIJI, UBANGIJI, ne ƙarfina da waƙata;
ya zama mai cetona.”
3 Da farin ciki zan ɗebo ruwa
daga rijiyoyin ceto.
4 A wannan rana za ku ce,
“Yi godiya ga UBANGIJI, ku kira bisa sunansa;
a sanar da wannan abin da ya aikata a cikin al’ummai,
a kuma yi shela cewa sunansa mai girma ne.
5 Ku rera ga UBANGIJI, gama ya aikata manyan abubuwa;
bari a sanar da wannan ga dukan duniya.
6 Ku tā da murya ku kuma rera don farin ciki, ya ku mutanen Sihiyona,
gama Mai Tsarki na Isra’ila da girma yake a cikinku.”

# 13

*Annabci a kan Babilon*

1 Abubuwan da Allah ya yi magana a kai game da Babilon da Ishaya ɗan Amoz ya
gani.
2 A tā da tuta a kan tudun da yake mai fili,
ka tā da murya gare su;
ka ɗaga hannu ka ba su alama
don su shiga ƙofofi masu alfarma.
3 Na umarci tsarkakana;
na umarci jarumawan yaƙina su gamsar da fushina,
waɗanda suke farin ciki a nasarata.

4 Ka saurara, akwai surutu a kan duwatsu,
sai ka ce na babban taron jama’a!
Ka saurara, akwai hayaniya a cikin mulkoki,
sai ka ce al’ummai ne suna ta tattaruwa!
UBANGIJI Maɗaukaki yana shirya
mayaƙa don yaƙi.
5 Suna zuwa daga ƙasashe masu nesa,
daga iyakokin duniya,
UBANGIJI da kuma fushinsa,
zai hallaka dukan ƙasar.

6 Ku yi ihu, gama ranar UBANGIJI ta yi kusa
za tă zo kamar hallaka daga Maɗaukaki.*
7 Saboda wannan, hannun kowane mutum zai yi rauni,
ƙarfin halin kowane mutum zai kāsa.
8 Tsoro zai kama su,

* **13:6** Da Ibraniyanci Shaddai

zafi da azaba za su ci ƙarfinsu;
za su yi ta murɗewa kamar mace mai naƙuda.
Za su dubi juna a tsorace,
fuskokinsu a ɓace.

9 Duba, ranar UBANGIJI tana zuwa,
muguwar rana, mai hasala da zafin fushi,
don ta mai da ƙasar kango
ta kuma hallakar da masu zunubi da suke cikinta.
10 Taurarin sama da ƙungiyoyinsu
ba za su ba da haskensu ba.
Rana za tă yi duhu
wata kuma ba zai ba da haskensa ba.
11 Zan hukunta duniya saboda muguntarta,
mugaye saboda zunubansu.
Zan kawo ƙarshe ga girman kan masu taƙama
in kuma ƙasƙantar da ɗaga kan marasa tausayi.
12 Zan sa mutum yă fi zinariya zalla wuyar samuwa,
fiye da zinariyar Ofir wuyan gani.
13 Saboda haka zan sa sammai su yi rawar jiki;
duniya kuma za tă girgiza daga inda take
a fushin UBANGIJI Maɗaukaki,
a ranar fushinsa mai ƙuna.

14 Kamar barewar da ake farautarta
kamar tumaki marasa makiyayi,
haka nan kowane mutum zai koma ga mutanensa,
kowane mutum zai gudu zuwa ƙasarsa.
15 Duk wanda aka kama za a soke shi yă mutu;
dukan waɗanda aka kama za su mutu ta takobi.
16 Za a fyaɗa ’ya’yansu a ƙasa su yi kucu-kucu a idanunsu;
za a washe gidajensu, a kuma kwana da matansu.

17 Duba, zan zuga mutanen Medes su yi gāba da su,
su da ba su kula da azurfa ba
kuma ba sa damuwa da zinariya.
18 Bakkunansu za su kashe samari;
ba za su ji tausayin jarirai ba
ba za su kuwa nuna jinƙai ga ’yan yara ba.
19 Babilon, kayan daraja na mulkoki,
abin fariyar Babiloniyawa,†
Allah zai kaɓantar da ita
kamar yadda ya yi da Sodom da Gomorra.
20 Ba za ƙara kasance da mazauna kuma ba
ko a yi zama a cikinta dukan zamanai;
Ba wani mutumin Arab da zai kafa tentinsa a can,
ba makiyayin da zai taɓa kiwon garkensa a can.
21 Amma halittun hamada za su kwanta a can,
diloli za su cika gidajenta;
a can mujiyoyi za su zauna,
a can kuma awakin jeji za su yi ta tsalle.

† **13:19** Ko kuwa Kaldiyawa

22 Kuraye za su yi ta kuka a kagarorinta,
diloli kuma a cikin fadodinta masu alfarma.
Lokacinta ya yi kusa,
kwanakinta kuma ba za su yi tsawo ba.

# 14

1 UBANGIJI zai yi wa Yaƙub jinƙai;
zai sāke zaɓi Isra'ila
yă kuma zaunar da su a ƙasarsu.
Baƙi ma za su zo su zauna tare da su
su haɗa kai da gidan Yaƙub.
2 Al'ummai za su ɗauke su
su kuma kawo wurin da yake nasu.
Gidan Isra'ila kuwa za tă mallaki al'ummai
a matsayin bayi maza da mata a ƙasar UBANGIJI.
Za su mai da waɗanda suka kama su su zama kamammu
su kuma yi mulki a kan waɗanda suka taɓa danne su.
3 A ranar da UBANGIJI ya hutashe ku daga wahala da azaba da muguwar bauta, 4 za
ku yi wa sarkin Babilon wannan ba'a.
Mai danniya ya zo ga ƙarshe!
Dubi yadda fushinsa ya ƙare!
5 UBANGIJI ya karye sandar mugaye,
sandan mulkin masu mulki,
6 wanda cikin fushi ya kashe mutane
da bugu marar ƙarewa,
kuma cikin fushi ya mamaye al'ummai
da fushi ba ƙaƙƙautawa.
7 Dukan ƙasashe suna hutawa suna kuma cikin salama;
sun ɓarke da waƙa.
8 Har itatuwan fir ma da kuma al'ul na Lebanon
suna murna a kanka suna cewa,
"Yanzu da aka ƙasƙantar da kai,
babu wani mai yankan katakon da ya zo yă yanka mu."

9 Kabari a ƙarƙashi duk ya shirya
don yă sadu da kai a zuwanka;
yana tā da ruhohin da suka rasu don su gaishe ka,
dukan waɗanda sun taɓa zama shugabanni a duniya;
ya sa suka tashi daga kujerun sarauta,
dukan waɗanda suke sarakuna a kan al'ummai.
10 Duk za su amsa,
za su ce maka,
"Ashe kai ma raunana ne, kamar mu;
ka zama kamar mu."
11 An yi ƙasa da dukan alfarmarka zuwa kabari,
tare da surutan garayunka;
tsutsotsi sun bazu a ƙarƙashinka
tsutsotsi kuma suka rufe ka.

12 Yaya aka yi ka fāɗo daga sama
Ya tauraron safiya, ɗan hasken asuba!

An fyaɗa ka da ƙasa,
kai da ka taɓa ƙasƙantar da al'ummai!
13 Ka yi tunani a ranka ka ce,
"Zan hau zuwa sama;
zan ɗaga kursiyina
sama da taurarin Allah;
zan zauna a kursiyi a kan dutsen taro,
a can ƙurewar saman dutse mai tsarki.*
14 Zan haura can bisa gizagizai;
zan mai da kaina kamar Mafi Ɗaukaka."
15 Amma ga shi an gangara da kai zuwa kabari,
zuwa zurfafan rami.

16 Waɗanda suka gan ka sun zura maka ido,
suna tunani abin da zai same ka.
"Wannan mutumin ne ya girgiza duniya
ya kuma sa mulkoki suka razana,
17 mutumin da ya mai da duniya ta zama hamada,
wanda ya tumɓuke biranenta
bai kuma bar kamammunsa suka tafi ba?"

18 Dukan sarakunan duniya suna kwance a mace,
kowa a kabarinsa.
19 Amma an jefar da kabarinka
kamar reshen da aka ƙi;
an rufe ka da waɗanda aka kashe,
tare da waɗanda aka soke da takobi,
waɗanda suka gangara zuwa duwatsun rami.
Kamar gawar da aka tattake da ƙafa,
20 ba za a haɗa ka tare da su a jana'iza ba,
gama ka hallaka ƙasarka
ka kuma kashe mutanenka.

Ba za a ƙara ambaci
zuriyarka masu aikata mugunta ba.
21 A shirya wuri don a yayyanka 'ya'yansa maza
saboda zunuban kakanninsu;
kada a reno su su gāji ƙasar
su cika duniya da biranensu.

22 "Zan yi gāba da su,"
in ji Ubangiji Maɗaukaki.
"Zan kau da sunan Babilon da waɗanda suka rage da rai a cikinta,
'ya'yanta da zuriyarta,"
in ji Ubangiji.

23 "Zan mai da ita wuri domin mujiyoyi
da kuma fadama;
zan share ta da tsintsiyar hallaka,"
Ni Ubangiji Maɗaukaki na faɗa.

* **14:13** Ko kuwa arewa; Da Ibraniyanci Zafon

*Annabci a kan Assuriya*

24 UBANGIJI Maɗaukaki ya rantse,
"Tabbatacce, kamar yadda na riga na shirya, haka zai kasance,
kuma kamar yadda na nufa, haka zai zama.
25 Zan ragargazar da Assuriya a cikin ƙasata;
a kan duwatsuna zan tattake shi.
Za a ɗauke nauyin da ya sa wa mutanena,
a kuma ɗauke nauyinsa daga kafaɗunsu."

26 Wannan shi ne shirin da na yi domin dukan duniya;
wannan shi ne hannun da aka miƙa a bisa dukan al'ummai ke nan.
27 Gama UBANGIJI Maɗaukaki ya ƙudura ya yi wannan, wa kuwa zai hana shi?
Ya riga ya miƙa hannunsa, wa zai komar da shi?

*Annabci a kan Filistiyawa*

28 Wannan abin da Allah ya yi magana ya zo ne a shekarar da Sarki Ahaz ya mutu.
29 Kada ku yi farin ciki, dukanku Filistiyawa,
cewa sandar da ta buge ku ta karye;
daga saiwar wannan maciji wani mugun maciji mai dafi zai taso,
'ya'yansa za su zama wani maciji masu dafi mai tashi sama.
30 Mafi talauci na matalauta zai sami wurin kiwo,
mabukata kuma za su kwana lafiya.
Amma zan hallakar da saiwarka da matsananciyar yunwa;
za tă kashe naka da suka rage da rai.

31 Ki yi ihu, ya ke ƙofa! Yi kururuwa, ya ke birni!
Ku razana, dukanku Filistiyawa!
Kunshin hayaƙi yana tasowa daga arewa,
kuma babu matsorata a cikin sojojinsa.
32 Wace amsa ce za a bayar
wa jakadun wannan al'umma?
"UBANGIJI ya kafa Sihiyona,
kuma a cikinta mutanensa masu shan azaba za su sami mafaka."

# 15

*Annabci a kan Mowab*

1 Abin da Allah ya yi magana a kan Mowab shi ne,
An lalatar da Ar a Mowab,
an hallaka ta da dare!
An lalatar da Kir a Mowab,
an hallaka ta da dare!
2 Dibon ya haura zuwa haikalinta,
zuwa masujadan kan tudu don tă yi kuka;
Mowab ta yi ihu a kan Nebo da Medeba.
An aske kowane kai
an kuma yanke kowane gemu.
3 A tituna sun sa tsummoki a jikunansu;
a kan rufin ɗakuna da kuma dandalin taruwa
dukansu sai makoki suke yi,
sun kwanta suna kuka.
4 Heshbon da Eleyale sun yi kuka da ƙarfi,
aka ji muryoyinsu ko'ina har zuwa Yahaz.

Saboda haka mayaƙan Mowab suka yi kuka da ƙarfi,
har zuciyarsu ta karai.

5 Zuciyata ta yi kuka a kan Mowab;
mutanenta sun gudu har zuwa Zowar,
har zuwa Eglat Shelishiya.
Sun haura zuwa Luhit,
suna tafe suna kuka;
a kan hanyar zuwa Horonayim
suna makoki saboda hallakawarsu.
6 Ruwayen Nimrim sun ƙafe
ciyayin kuma sun bushe;
tsire-tsire duk sun ɓace
babu sauran ɗanyen abu.
7 Saboda haka dukiyar da suka tara suka kuma ajiye
sun ɗauka suka ƙetare Rafin Arabim da su.
8 Kugin kukansu ya kai ko'ina a iyakar Mowab;
kururuwarsu ta kai har zuwa Eglayim,
makokinsu ya kai har zuwa Beyer-Elim.
9 Ruwayen Dimon sun cika da jini,
amma zan yi ƙari a kan Dimon,
zan kawo zaki a kan masu gudu na Mowab
da kuma a kan waɗanda suka ragu a ƙasar.

# 16

1 Ku aiko da raguna a matsayin haraji
ga mai mulkin ƙasar,
daga Sela a hamada,
zuwa dutsen Diyar Sihiyona.
2 Kamar tsuntsaye masu firiya
da aka kora daga sheƙa,
haka matan Mowab suke
a kogunan Arnon.

3 "Ku ba mu shawara,
ku yanke shawara.
Ku mai da inuwarku kamar dare,
a tsakar rana.
Ku ɓoye masu gudun hijira,
kada ku bashe masu neman mafaka.
4 Ku bar Mowabawa masu gudun hijira su zauna tare da ku;
ku zama mafakarsu daga mai neman hallaka su."

Mai danniya zai zo ga ƙarshe
hallaka kuma za tă daina;
masu lalatar da ƙasa za su kare
5 Da ƙauna za a kafa kursiyi;
da aminci mutum zai zauna a kansa,
wani daga gidan* Dawuda,

* 16:5 Da Ibraniyanci tenti

wani wanda ta shari’antawa yakan nuna gaskiya
ya hanzarta yin adalci.

6 Mun ji fariyar Mowab,
mun ji yawan fariyarta da girmankanta,
fariyarta da reninta,
amma taƙamarsu ta banza ce.
7 Saboda haka Mowabawa za su yi kuka mai zafi,
za su yi kuka mai zafi tare saboda Mowab.
Ku yi makoki ku kuma yi baƙin ciki
saboda ƙosai da kuka riƙa ci a Kir Hareset.
8 Gonakin Heshbon sun bushe,
inabin Sibma ma haka.
Masu mulkin al’ummai
sun tattake inabi mafi kyau,
waɗanda suka taɓa yaɗuwa zuwa Yazer
suka bazu ta wajen hamada.
Tohonsu sun buɗu
suka kai har teku.
9 Saboda haka na yi kuka, yadda Yazer take kuka,
saboda inabin Sibma.
Ya Heshbon, ya Eleyale,
na cika ku da hawaye!
Sowa ta murna a kanku saboda ’ya’yan itatuwanku da suka nuna
da kuma girbinku sun ɓace.
10 An ɗauke farin ciki da murna daga gonakin itatuwa masu ’ya’ya;
babu wanda yake rerawa ko yake sowa a cikin gonakin inabi;
babu wanda yake matsin ruwan inabi a wuraren matsi,
gama na kawo ƙarshen yin sowa.
11 Zuciyata tana makoki saboda Mowab kamar garaya,
na yi baƙin ciki saboda Kir Hareset.
12 Sa’ad Mowab ta bayyana a masujadar bisa tudu,
tana gajiyar da kanta ne kawai;
sa’ad da ta tafi wurin tsafinta don tă yi addu’a,
babu wani amfani.
13 Wannan ita ce maganar da Ubangiji ya riga ya yi game da Mowab. 14 Amma
yanzu Ubangiji ya ce, “Cikin shekara uku, kamar yadda bawan da aka bautar da
shi bisa ga yarjejjeniya zai lissafta, haka za a mai da daraja da kuma dukan yawan
mutanen Mowab abin reni, daga ɗumbun mutanenta, ’yan kaɗan ne kaɗai za su
ragu, za su kuma zama marasa ƙarfi.”

# 17

*Abin da Allah ya faɗa a kan Damaskus*

1 Abin da Allah ya faɗa game da Damaskus.
“Duba, Damaskus ba za tă ƙara zama birni ba
amma za tă zama tsibin juji.
2 Za a watse a bar biranen Arower
a bar wa tumaki da shanu, waɗanda za su kwanta,
ba tare da wani wanda zai tsorata su ba.
3 Birni mai katanga za tă ɓace daga Efraim,
ikon sarauta kuma daga Damaskus;
raguwar Aram za tă zama

kamar darajar Isra'ila,"
in ji UBANGIJI Maɗaukaki.

4 "A wannan rana ɗaukakar Yaƙub za tă ƙare;
kitsen jikinsa zai lalace.
5 Zai zama kamar sa'ad da mai girbi ya tara hatsin da yake tsaye
ya kuma girbe hatsin da hannunsa
kamar sa'ad da mutum ya yi kala kawunan hatsi
a Kwarin Refayim.
6 Duk da haka waɗansu kala za su ragu,
sai ka ce sa'ad da an karkaɗe itace zaitun,
aka bar 'ya'yan zaitun biyu ko uku a can ƙwanƙolin rassan,
ko kuma aka bar huɗu ko biyar a rassa na gefe na itace mai 'ya'ya,"
in ji UBANGIJI, Allah na Isra'ila.

7 A wannan rana mutane za su nemi Mahaliccinsu
su kuma juye idanunsu ga Mai Tsarkin nan na Isra'ila.
8 Ba za su dubi bagade ba,
waɗanda suke aikin hannuwansu,
ba za su kuma kula da ginshiƙan Ashera ba*
da kuma bagadan turaren da yatsotsinsu suka yi.
9 A wannan rana biranensu masu ƙarfi, waɗanda suka bari saboda Isra'ilawa, za su
zama kamar wuraren da aka ƙyale suka zama kufai a jeji. Za su kuma zama kango.
10 Kun manta da Allah Mai Cetonku;
ba ku tuna da Dutse, kagararku ba.
Saboda haka, ko da yake kun fita ku shuka tsire-tsire mafi kyau
kuka kuma shuka inabin da aka sayo daga waje,
11 ko da yake a ranar kun shuka su, kuka sa su yi girma,
da safe kuma sa'ad da kuka shuka su, kuka sa suka yi toho suka yi fure,
duk da haka girbin ba zai zama kome ba
a ranar cuta da zafin da ba ta da magani.

12 Kash, ga hayaniyar al'ummai masu yawa
suna hayaniya kamar rurin teku!
Kash, ga fushin mutane
suna ruri kamar rugugi kamar manyan ruwaye!
13 Ko da yake mutane suna ruri kamar sukuwar raƙuman ruwa,
sa'ad da ya tsawata musu za su gudu can da nisa,
aka kore su kamar yayinda iska ya hura a kan tuddai,
kamar tattake kuma a cikin guguwa.
14 Da yamma, sai razana ba tsammani!
Kafin safiya, duk sun ɓace!
Wannan ne rabon waɗanda suka washe mu,
rabon waɗanda suka yi mana ƙwace.

# 18

*Annabci a kan Kush*

1 Kaiton ƙasar da ake jin ƙarar fikafikai*
a bakin kogunan Kush,†

* **17:8** Wato, alamun alliya Ashera. * **18:1** Ko kuwa na fari † **18:1** Wato, yankin Nilu na Bisa

2 wadda ta aiko da jakadu ta teku
cikin jiragen ruwan da aka yi da kyauro a bisa ruwa.

Ku tafi, ku ʼyan saƙo masu sauri,
zuwa ga dogayen mutane masu sulɓin jiki,
zuwa ga mutanen da ake jin tsoro a koʼina,
alʼumma mai ƙarfin iko tana jawabin da ba a saba ji ba,
mai ƙasar da koguna suka raba.

3 Ku dukan mutanen duniya,
ku da kuke zama a duniya,
saʼad da aka ɗaga tutar a kan duwatsu,
za ku gan shi,
saʼad da kuma aka busa ƙaho,
za ku ji shi.
4 Ga abin da UBANGIJI ya faɗa mini,
"Zan yi shiru in kuma duba a hankali daga mazaunina,
kamar ƙuna mai zafi a hasken rana,
kamar girgijen raba a lokacin girbi."
5 Gama kafin girbi, saʼad da furanni suka karkaɗe
furanni kuma suka zama ʼyaʼyan inabin da suka nuna,
zai faffalle rassan kuringar inabi da wuƙa,
ya yanke ya kuma kwashe rassan da suka bazu.
6 Duk za a bar su wa tsuntsayen dutse su ci
da kuma namun jeji;
tsuntsaye kuma za su ci rani a kansu,
namun jeji kuma za su yi damina a kansu.
7 A wannan lokaci za a kawo kyautai wa UBANGIJI Maɗaukaki
daga dogayen mutane masu sulɓin jiki,
daga mutanen da ake jin tsoro a koʼina,
alʼumma mai ƙarfin iko na jawabin da ba a saba ji ba,
mai ƙasar da koguna suka raba.
Za a kawo kyautai zuwa Dutsen Sihiyona, wurin da Sunan UBANGIJI Maɗaukaki yake.

# 19

*Annabci a kan Masar*

1 Abin da Allah ya faɗa game da Masar,
Duba, UBANGIJI yana a kan girgije a sukwane
yana kuwa zuwa Masar.
Gumakan Masar sun firgita a gabansa,
zukatan Masarawa sun karai.

2 "Zan tā da hargitsi tsakanin mutumin Masar da mutumin Masar,
ɗanʼuwa zai yi gāba da ɗanʼuwa
maƙwabci ya yi gāba da maƙwabci,
birni ya yi gāba da birni,
mulki ya yi gāba da mulki.
3 Masarawa za su karai,
zan kuma sa shirye-shiryensu su zama banza;
za su nemi shawarar gumaka da kuma ruhohin matattu,
za su nemi shawarar mabiya da na masu duba.

4 Zan ba da Masarawa
ga ikon azzalumi shugaba,
mugun sarki kuma zai yi mulki a kansu,"
in ji mai girma, UBANGIJI Maɗaukaki.

5 Ruwayen kogi za su ƙafe,
bakin kogi zai shanye yă kuma bushe.
6 Wuriyoyi za su yi wari;
rafuffukan Masar za su yi ta raguwa har su ƙafe.
Iwa da jema za su bushe,
7 haka ma tsire-tsire kusa da Nilu,
a bakin kogi.
Kowane abin da aka shuka a gefen Nilu
zai bushe, iska ta kwashe su ƙaf.
8 Masu kamun kifi za su yi nishi su kuma yi makoki,
dukan waɗanda suke jefan ƙugiyoyi a Nilu;
waɗanda suke jefan abin kamun kifi a ruwa
abin kamun kifin za su zama marasa amfani.
9 Waɗanda suke aiki da kaɗin auduga za su karai,
masu yin lilin mai kyau za su fid da zuciya.
10 Masu aikin tufafi ransu zai ɓace,
kuma dukan masu samun albashi za su damu.

11 Shugabannin Zowan ba kome ba ne, wawaye ke kawai;
mashawarta masu hikima na Fir'auna suna ba da shawarwari marasa amfani.
Yaya za ka ce wa Fir'auna,
"Ni ɗaya ne cikin masu hikima,
almajirin sarakuna na dā can"?

12 Ina masu hikima suke yanzu?
Bari su nuna maka su kuma sanar
da abin da UBANGIJI Maɗaukaki
ya shirya a kan Masar.
13 Shugabannin Zowan sun zama wawaye,
an ruɗe shugabannin Memfis*
dutsen kan kusurwa na mutanenta
su sa Masar ta kauce.
14 UBANGIJI ya sa zuba musu
ruhun jiri;
suka sa Masar ta yi tangaɗi cikin kome da take yi,
kamar yadda mutumin da ya bugu yake tangaɗi cikin amansa.
15 Babu abin da Masar za tă yi,
kai ko wutsiya, reshen dabino ko iwa.
16 A wannan rana Masarawa za su zama kamar mata. Za su yi rawar jiki lokacin
da UBANGIJI Maɗaukaki ya ɗaga hannu a kansu. 17 Kasar Yahuda kuma za kawo
fargaba ga Masarawa; kowanne da Yahuda ya ambace zai firgita, saboda abin da
UBANGIJI Maɗaukaki yake shiri a kansu.
18 A wannan rana birane biyar a Masar za su yi yaren Kan'ana su kuma miƙa kai
cikin yarjejjeniya ga UBANGIJI Maɗaukaki. Za a ce da ɗayansu Birnin Hallaka.

* **19:13** Da Ibraniyanci Nof

[19] A wannan rana za a kasance da bagade ga UBANGIJI a tsakiyar Masar, da kuma
ginshiƙin dutse UBANGIJI a iyakarta. [20] Zai zama alama da kuma shaida ga UBANGIJI
Maɗaukaki a ƙasar Masar. Sa'ad da suka yi kuka ga UBANGIJI saboda masu zaluntarsu,
zai aiko musu mai ceto da mai kāriya, zai kuma cece su. [21] Saboda haka UBANGIJI zai
sanar da kansa ga Masarawa, kuma a wannan rana za su yarda da UBANGIJI. Za su
yi masa sujada da hadayu da hadayun hatsi; za su yi alkawura ga UBANGIJI su kuma
kiyaye su. [22] UBANGIJI zai bugi Masar da annoba; zai buge su ya kuma warkar da su.
Za su juyo wurin UBANGIJI, zai amsa roƙonsu ya kuma warkar da su.
[23] A wannan rana za a kasance da babban hanya daga Masar zuwa Assuriya.
Assuriyawa za su tafi Masar, Masarawa kuma za su tafi Assuriya. Masarawa da
Assuriyawa za su yi sujada tare. [24] A wannan rana Isra'ila za tă zama na uku, tare
da Masar da Assuriya, abin albarka ga duniya. [25] UBANGIJI Maɗaukaki zai albarkace
su, yana cewa, "Albarka ta tabbata ga Masar, mutanena, Assuriya aikin hannuna, da
kuma Isra'ila gādona."

# 20

*Annabci a kan Masar da Kush*

[1] A shekarar da babban shugaban yaƙin da Sargon sarkin Assuriya ya aika, ya zo
Ashdod ya kuma fāɗa mata ya kuma ci ta da yaƙi, [2] a wannan lokaci UBANGIJI ya yi
magana ta wurin Ishaya ɗan Amoz. Ya ce masa, "Tuɓe tsummokin da kake saye da
su, da kuma takalman da ka sa a ƙafafu." Ya kuwa yi haka, yana yawo tsirara kuma
ba takalma a ƙafa.
[3] Sa'an nan UBANGIJI ya ce, "Kamar dai yadda bawana Ishaya ya yi ta yawo tsirara
kuma ba takalmi a ƙafa shekara uku, a matsayin alama da shaida a kan Masar da
Kush,* [4] haka sarkin Assuriya zai kwashe kamammun Masarawa da Kushawa tsirara
kuma ba takalma a ƙafa, yaro da babba, asirinsu a tsiraice, don a kunyata Masar.
[5] Waɗanda suka dogara ga Kush suka yi taƙama da Masar za su ji tsoro su kuma sha
kunya. [6] A wannan rana mutanen da suke zama a bakin teku za su ce, 'Dubi abin da
ya faru da waɗanda muka dogara a kai, waɗanda muka gudu muka je don neman
taimako da ceto daga sarkin Assuriya! Yaya za mu tsira?' "

# 21

*Annabci a kan Babilon*

[1] Abin da Allah ya faɗa game da Hamada da take kusa da Teku.
Kamar guguwa mai share cikin ƙasar kudu,
mai hari ya zo daga hamada,
daga ƙasar mai banrazana.

[2] An nuna mini mugun wahayi,
mai bashewa ya bashe, mai washewa ya washe.
Elam, ki yi yaƙi! Mediya, ki yi kwanto!
Zan kawo ƙarshen dukan nishe-nishen da ta jawo.

[3] Game da wannan jikina yana ciwo,
zafi ya kama ni, kamar na mace mai naƙuda;
na razana game da abin da na ji,
na yi mamakin abin da na gani.
[4] Gabana tana ta fāɗuwa,
tsoro ya sa ina rawan jiki;

* **20:3** Wato, yankin Nilu na Bisa; haka ma a aya 5

hasken da nake marmari
ya zo da razana gare ni.

5 Sun shirya teburori,
sun shimfiɗa dardumai,
sun ci, sun sha!
Tashi, ku hafsoshi,
sa mai a garkuwoyi!
6 Ga abin da mai girma ya ce mini,
"Tafi, ka sa mai tsaro
ka kuma sa ya ba da rahoton abin da ya gani.
7 Sa'ad da ya ga kekunan yaƙi
tare da ƙungiyoyin dawakai,
mahaya a kan jakuna,
ko mahaya a kan raƙuma,
to, fa ya zauna a faɗake,
ya kintsa sosai."
8 Mai tsaron kuma ya yi ihu,
"Kowace rana, ranka yă daɗe, nakan tsaya a hasumiyar tsaro;
kowane dare nakan tsaya a wurin aikina.
9 Duba, ga wani mutum tafe a keken yaƙin
tare da ƙungiyar dawakai.
Ya kuma mayar da amsa,
'Babilon ta fāɗi, ta fāɗi!
Dukan siffofin allolinta
kwance a ragargaje a ƙasa!' "

10 Ya mutanena, an ragargaje ku a masussuka,
na faɗa muku abin da na ji
daga UBANGIJI Maɗaukaki,
daga Allah na Isra'ila.

### *Annabci a kan Edom*

11 Abin da Allah ya faɗa game da Duma,*
Wani ya kira ni daga Seyir,
"Mai tsaro, me ya rage a daren?
Mai tsaro, me ya rage a daren?"
12 Mai tsaro ya amsa,
"Safiya ta gabato, haka kuma dare.
In za ka yi tambaya, to, yi tambaya;
sai ka sāke zuwa, ka tambaya."

### *Annabci a kan Arabiya*

13 Abin da Allah ya faɗa game da Arabiya.
Ku ayarin Dedanawa,
ku da kuka sauka a jejin Arabiya,
14 ku kawo ruwa don ƙishirwa;
ku da kuke zama a Tema,
ku kawo abinci don masu gudun hijira.
15 Sun gudu daga takobi,
daga takobin da aka janye,

* **21:11** Duma yana nufin shiru Ko kuwa natsattse, wani sunan Edom.

daga bakan da aka tanƙware
da kuma daga zafin yaƙi.
16 Ga abin da mai girma ya ce mini, “Cikin shekara ɗaya, kamar yadda bawan da
aka bautar da shi bisa ga yarjejjeniya zai lissafta, dukan sojojin Kedar za su zo ga
ƙarshe. 17 Waɗanda suka yi rai na maharba, jarumawan Kedar, za su zama kaɗan.”
UBANGIJI, Allah na Isra’ila, ya faɗa.

# 22

*Annabci a kan Urushalima*

1 Abin da Allah ya faɗa game da Kwarin Wahayi.
Mene ne ya dame ku a yanzu,
da dukanku kuka hau kan rufin gidaje.
2 Ya kai gari cike da hayaniya,
Ya ke birnin tashin hankali da alkarya mai murna?
Mutanenki ba su mutu ta wurin takobi ba,
ba kuwa za su mutu a yaƙi ba.
3 Dukan shugabanninki sun gudu gaba ɗaya;
an kama su ba tare da an yi amfani da baka ba.
Dukanku da aka kama an kwashe ku ɗaurarru gaba ɗaya,
kun gudu tun abokin gāba yana da nisa.
4 Saboda haka na ce, “Kyale ni kurum;
bari in yi kuka mai zafi.
Kada ka yi ƙoƙarin ta’azantar da ni
a kan hallakar mutanena.”

5 Ubangiji, UBANGIJI Maɗaukaki, yana da ranar
giggicewa da tattakewa da banrazana
a cikin Kwarin Wahayi,
ranar ragargazawar katanga
da ta yin kuka ga duwatsu.
6 Elam ya ɗauki kwari da baka,
tare da mahayan kekunan yaƙinta da dawakai;
Kir ta buɗe garkuwoyi.
7 Kwarurukanku mafi kyau sun cika da kekunan yaƙi,
an kuma tsai da mahayan dawakai a ƙofofin birni.

8 An rurrushe kāriyar Yahuda,
a ranan nan kuwa kun yi la’akari
da makamai a cikin Fadan Kurmi;
9 kuka ga cewa Birnin Dawuda
tana da wuraren kāriya masu yawa da suka tsattsage;
kuka tattara ruwa
a Tafkin Kasa.
10 Kuka ƙirga gine-gine a Urushalima
kuka kuma rurrushe gidaje don ku ƙarfafa katanga.
11 Kuka gina matarar ruwa tsakanin katanga biyu
saboda ruwan Tsohon Tafki,
amma ba ku yi la’akari da Wannan da ya yi su ba,
ko ku kula da Wannan da ya shirya shi tuntuni.

12 Ubangiji, UBANGIJI Maɗaukaki

ya kira ku a wannan rana
don ku yi kuka ku yi ihu,
don ku aske gashinku ku kuma sa tsummoki.
13 Amma duba, sai ga shi kuna farin ciki kuna kuma murna,
kuna yankan shanu kuna kashe tumaki,
kuna cin nama kuna kuma shan ruwan inabi!
Kuna cewa, “Bari mu ci mu kuma sha,
gama gobe za mu mutu!”
14 UBANGIJI Maɗaukaki ya bayyana wannan a kunnena cewa, “Har ranar mu-
tuwarka ba za a yi kafarar wannan zunubi ba,” in ji mai girma UBANGIJI Maɗaukaki.
15 Ga abin da Ubangiji, UBANGIJI Maɗaukaki, ya faɗa,
“Je, ka faɗa wa wannan mai hidima,
Shebna, sarkin fada.
16 Mene ne kake yi a nan kuma wa ya ba ka izini
ka haƙa kabari wa kanka a nan,
kana fafe kabarinka a bisa
kana sassaƙa wurin hutunka a dutse?

17 “Ka yi hankali, UBANGIJI yana shirin ya kama ka da ƙarfi
ya kuma ɗauke ka, ya kai mai ƙarfi.
18 Zai dunƙule ka kamar ƙwallo
ya jefa ka a cikin ƙasa mai girma.
A can za ka mutu
a can kuma kekunan yaƙinka masu daraja za su kasance,
abin kunya kake ga gidan maigidanka!
19 Zan tumɓuke ka daga makaminka,
za a kuma kore ka daga matsayinka.
20 “A wannan rana zan kira bawana, Eliyakim ɗan Hilkiya. 21 Zan rufe shi da
rigarka in kuma yi masa ɗamara in miƙa masa ikonka. Zai zama mahaifi ga waɗanda
suke zama a Urushalima da kuma gidan Yahuda. 22 Zan sa mabuɗin gidan Dawuda
a kafaɗarsa; abin da ya buɗe ba mai rufewa, kuma abin da ya rufe ba mai buɗewa.
23 Zan kafa shi kamar turke a tsayayyen wuri; zai zama mazaunin* daraja domin
gidan mahaifinsa. 24 Dukan ɗaukakar iyalinsa za tă rataya a kansa daga ’ya’yansa
da zuriyarsa har zuwa dukan ƙananan kayan aikinsa, wato, daga kwanoni har zuwa
tuluna.
25 “A ranan nan, in ji UBANGIJI Maɗaukaki, turken da aka kafa a tsayayyen wuri zai
sumɓule; za a sare shi ya fāɗi, za a kuma datse nauyin da yake rataya a kansa.” Ni
UBANGIJI na faɗa.

# 23

*Annabci a kan Taya*

1 Abin da Allah ya faɗa game da Taya.
Ku yi kuka mai zafi, ya jiragen ruwan Tarshish!
Gama an hallaka Taya
aka kuma bar su babu gida ko tasha.
Daga ƙasar Saifurus*
magana ta zo musu.

2 Ku yi shiru, ku mutanen tsibiri
da ku ’yan kasuwan Sidon

* **22:23** Ko kuwa kursiyi * **23:1** Da Ibraniyanci Kittim

wadanda masu ciniki a teku suka azurta.
3 A manyan ruwaye
hatsin Shihor suka iso;
girbin Nilu ne kuɗin shiga na Taya
ta kuma zama kasuwar al'ummai.

4 Ki ji kunya, ya ke Sidon, da ke kuma, kagarar teku,
gama teku ya yi magana ya ce,
"Ban taɓa naƙuda ba balle in haifi 'ya'ya;
ban taɓa goyon 'ya'ya maza ba balle in reno 'ya'ya mata."
5 Sa'ad da magana ta kai Masar,
za su razana da jin labari daga Taya.

6 Ku haye zuwa Tarshish;
ku yi kuka mai zafi, ku mutanen tsibiri.
7 Wannan ce birnin murnanku,
birnin nan na tun dā
wadda ƙafafunta suka kai ta
zama a ƙasashe masu nesa?
8 Wane ne ya ƙulla wannan a kan Taya
ita da take ba da rawanin sarauta,
wadda 'yan kasuwanta sarakuna ne,
wadda masu cinikinta sanannu ne a duniya?
9 Ubangiji Maɗaukaki ya ƙulla shi,
don yǎ kawo ƙarshen girman kan dukan darajarta
ya kuma ƙasƙantar da dukan waɗanda suke sanannu a duniya.

10 Ki nome ƙasarki har zuwa wajen Nilu,
Ya Diyar Tarshish,
gama ba ki da tashan jirgin ruwa kuma.
11 Ubangiji ya miƙa hannunsa a bisa teku
ya kuma sa mulkokinsa suka yi rawar jiki.
Ya ba da umarni game da Funisiya†
cewa a hallaka kagararta.
12 Ya ce, "Ba za ki ƙara yin murna ba,
Ya ke Budurwa Diyar Sidon, yanzu da kike ragargajiya!

"Tashi, ki ƙetare zuwa Saifurus;
a can ɗin ma ba za ki huta ba."
13 Dubi ƙasar Babiloniyawa,‡
wannan mutanen da yanzu ba su da wani amfani!
Assuriyawa sun mai da ita
wurin zaman halittun hamada;
sun gina hasumiyoyin kwanto,
suka ragargaza kagararta ƙaf
suka mai da ita kango.

14 Ku yi kuka mai zafi, ku jiragen ruwan Tarshish;
an rurrushe kagararku!

† **23:11** Da Ibraniyanci Kan'ana ‡ **23:13** Ko kuwa Kaldiyawa

[15] A wannan lokaci za a manta da Taya har shekaru saba'in, tsawon rayuwar sarki.
Amma a ƙarshen waɗannan shekaru saba'in, zai zama wa Taya kamar yadda yake
a waƙar karuwa cewa,
[16] "Ɗauki garaya, ki ratsa birni,
Ya ke karuwar da aka manta da ita;
kaɗa garaya da kyau, ki rera waƙoƙi masu yawa,
saboda a tuna da ke."
[17] A ƙarshen shekaru saba'in, UBANGIJI zai magance Taya. Za tă koma ga aikinta na
karuwanci za tă kuma yi kasuwancinta da dukan mulkokin duniya. [18] Duk da haka
za a keɓe ribarta da kuɗin shigarta wa UBANGIJI; ba za a yi ajiyarsu ko a ɓoye su.
Ribarta za tă tafi ga waɗanda suke yi wa UBANGIJI sujada, don su sami yalwataccen
abinci da tufafi masu kyau.

# 24

*Yin kaca-kaca da duniyar da UBANGIJI zai yi*

[1] Duba, UBANGIJI zai wofinta duniya
ya kuma yi kaca-kaca da ita;
zai ɓata fuskarta
ya watsar da mazaunanta,
[2] zai zama abu ɗaya
ga firist kamar yadda yake ga mutane,
ga maigida kamar yadda yake ga bawa,
ga uwargijiya kamar yadda yake ga baiwa,
ga mai sayarwa kamar yadda yake ga mai saya,
ga mai karɓan rance kamar yadda yake ga mai ba da rance,
ga mai karɓan bashi kamar yadda yake ga mai ba da bashi.
[3] Za a wofinta duniya ƙaƙaf
a kuma washe ta sarai.
UBANGIJI ne ya faɗa haka.

[4] Duniya ta bushe ta kuma yanƙwane,
duniya tana shan azaba ta kuma raunana,
masu daraja na duniya suna shan azaba.
[5] Duniya ta ƙazantu ta wurin mutanenta
sun ƙi yin biyayya da dokoki,
sun keta farillai
suka kuma karya madawwamin alkawari.
[6] Saboda haka la'ana za tă auko wa duniya;
dole mutanenta su ɗauki hakkin laifinsu.
Saboda haka aka ƙone mazaunan duniya,
kuma kaɗan ne kurum suka rage.
[7] Sabon ruwan inabi ya bushe kuringar inabi kuma sun yanƙwane;
dukan masu farin ciki suna nishi.
[8] Kaɗe-kaɗen garayu sun yi shiru,
surutun masu murna ya daina,
garayan farin ciki ya yi shiru.
[9] Babu sauran shan ruwan inabi suna rera waƙa;
barasa ya zama da ɗaci ga masu shanta.
[10] Birnin da aka birkice ta zama kango;
an kulle ƙofar shiga kowane gida.
[11] A lituna suna kukan neman ruwan inabi;

dukan farin ciki ya dawo baƙin ciki,
an hana dukan kaɗe-kaɗe a duniya.
12 An bar birnin kango,
aka yi kaca-kaca da ƙofofinta.
13 Haka zai zama a duniya
da kuma a cikin al'ummai,
kamar sa'ad da akan karkaɗe itacen zaitun,
ko kuma kamar sa'ad da ake barin kala bayan an girbe inabi.

14 Sun daga muryoyinsu, sun yi sowa ta farin ciki;
daga yamma sun furta darajar UBANGIJI.
15 Saboda haka a gabas sun ɗaukaka UBANGIJI,
a ɗaukaka sunan UBANGIJI, Allah na Isra'ila,
a cikin tsibiran teku.
16 Daga iyakokin duniya mun ji waƙoƙi,
"Ɗaukaka ga Mai Adalcin nan."

Amma na ce, "Na lalace, na lalace!
Kaitona!
Munafukai sun ci amana!
Da munafunci munafukai sun ci amana!"
17 Razana da rami da tarko suna jiranku,
Ya mutanen duniya.
18 Duk wanda ya yi ƙoƙarin tserewa daga ƙarar razana
zai fāɗa cikin rami;
wanda kuma ya tsere daga rami
za a kama shi a tarko.

An buɗe ƙofofin ambaliyar ruwan sama,
harsashen ginin duniya suna rawa.
19 An tsage duniya,
duniya ta farfashe ta wage,
an girgiza duniya ƙwarai.
20 Duniya tana tangaɗi kamar mashayi,
tana lilo kamar rumfa a cikin iska;
laifin tayarwarta ya yi nauyi sosai
har ta fāɗi ba kuwa za tă ƙara tashi ba.

21 A wannan rana UBANGIJI zai hukunta
ikokin da suke cikin sama
da kuma sarakunan da suke a duniya.
22 Za a tattara su tare
kamar ɗaurarru a kurkuku;
za a rufe su a kurkuku
a kuma hukunta su* bayan kwanaki masu yawa.
23 Sa'an nan wata zai ruɗe, rana ta ji kunya;
gama UBANGIJI Maɗaukaki zai yi mulki
a kan Dutsen Sihiyona da kuma a cikin Urushalima,
da kuma a gaban dattawanta, da ɗaukaka.

* **24:22** Ko kuwa a sāke su

# 25

*Yabo ga UBANGIJI*

1 Ya UBANGIJI, kai ne Allahna; zan ɗaukaka ka in kuma yabi sunanka,
gama cikin cikakken aminci ka yi abubuwa masu banmamaki,
abubuwan da aka shirya tun da.
2 Ka mai da birnin tsibin tarkace,
ka lalatar da gari mai katanga,
birnin baƙi mai ƙarfi, ta ɓace; ba za a ƙara gina ta ba.
3 Saboda haka mutane masu ƙarfi za su girmama ka;
biranen mugayen al'ummai za su ji tsoronka.
4 Kai ka zama mafakar matalauta, mafaka don mabukata cikin damuwa,
wurin ɓuya daga hadari, inuwa kuma daga zafin rana.
Gama numfashin mugaye yana kamar da hadari mai bugun bango
5 kuma kamar zafin hamada.
Ka kwantar da hayaniyar baƙi;
kamar yadda inuwar girgije kan rage zafin rana, haka ake kwantar da waƙar mugaye.

6 A kan wannan dutse UBANGIJI Maɗaukaki zai shirya bikin abinci mai kyau don dukan mutane,
liyafar ajiyayyen ruwan inabi da nama mafi kyau da ruwan inabi mafi kyau.
7 A wannan dutse zai kawar da
baƙin cikin da ya lulluɓe dukan mutane,
ƙyallen da ya rufe dukan al'ummai;
8 zai haɗiye mutuwa har abada.
UBANGIJI Mai Iko Duka zai share hawaye
daga dukan fuskoki;
zai kawar da kunyar mutanensa
daga dukan duniya.
UBANGIJI ne ya faɗa.
9 A wannan rana za su ce,
"Tabbatacce wannan shi ne Allah;
mun dogara a gare shi, ya kuma cece mu.
Wannan shi ne UBANGIJI, mun dogara a gare shi;
bari mu yi murna mu kuma yi farin ciki a cikin cetonsa."

10 Hannun UBANGIJI zai zauna a kan wannan dutse;
amma za a tattake Mowab a ƙarƙashinsa
kamar yadda ake tattaka kara a cikin taki.
11 Za su buɗe hannuwansa a cikinsa,
yadda mai iyo kan buɗe hannuwansa don yǎ yi iyo.
Allah ya ƙasƙantar da girmankansu
duk da wayon* hannuwansu.
12 Zai rurrushe manyan katangar kagaru
ya kuma ƙasƙantar da su;
zai rushe su har ƙasa,
su zama ƙura.

# 26

*Waƙar yabo*

* **25:11** Ma'anar kalmar Ibraniyancin nan babu tabbas.

1 A wannan rana za a rera wannan waƙa a ƙasar Yahuda.
Muna da birni mai ƙarfi;
Allah yake ceton
katanga da kuma kagarunta.
2 A buɗe ƙofofi
saboda al'umma mai adalci ta shiga,
al'ummar da mai aminci.
3 Za ka kiyaye shi da cikakken salama
shi wanda ya kafa zuciyarsa gare ka,
domin ya dogara a gare ka.
4 Ku dogara ga UBANGIJI,
gama shi UBANGIJI, ne madawwamin Dutse.
5 Yakan ƙasƙantar da waɗanda suke zama a bisa
ya kawar da birni mai alfarma ƙasa;
ya rusa ta har ƙasa
ya jefar da ita cikin ƙura.
6 Kafafu sukan tattake ta,
ƙafafu waɗanda aka zalunta,
wato, sawun matalauta.

7 Hanyar masu adalci sumul take;
Ya Mai Aikata Gaskiya, ka sa hanyar masu adalci ta yi sumul.
8 I, UBANGIJI, cikin tafiya a hanyar dokokinka,*
muna sa zuciya gare ka;
sunanka da tunani a kanka
su ne marmarin zukatanmu.
9 Raina yana marmarinka da dare;
da safe kuma raina yana son ganinka.
Sa'ad da hukunce-hukuncenka suka sauko duniya,
mutanen duniya kan koyi adalci.
10 Ko da yake akan nuna wa mugaye alheri,
ba sa koyi adalci;
har ma a ƙasar masu aikata gaskiya sukan ci gaba da aikata muguntа
ba sa ganin girmar darajar UBANGIJI.
11 Ya UBANGIJI an ɗaga hannunka sama,
amma ba sa ganinsa.
Bari su ga himmarka don mutanenka su kuma sha kunya;
bari wutar da aka ajiye don abokan gābanka ta cinye su.

12 UBANGIJI ka kafa salama dominmu;
duk abin da muka iya yi kai ne ka yi mana.
13 Ya UBANGIJI, Allahnmu, waɗansu iyayengiji ban da kai sun yi mulki a kanmu,
amma sunanka kaɗai muka girmama.
14 Yanzu duk sun mutu, ba za su ƙara rayuwa ba;
waɗannan ruhohin da suka rasu ba za su tashi ba.
Ka hukunta su ka kuma kawo su ga hallaka;
ka sa ba za a ƙara tunawa da su ba.
15 Ka fadada al'umma, ya UBANGIJI;
ka fadada al'umma.
Ka samo wa kanka ɗaukaka;
ka fadada dukan iyakokin ƙasar.

* **26:8** Ko kuwa hukunce-hukunce

16 UBANGIJI, sun zo gare ka a cikin damuwarsu;
sa'ad da ka hore su,
da ƙyar suna iya yin addu'a.†
17 Kamar mace mai ciki da take gab da haihuwa
takan yi ta murɗawa tana kuka saboda zafi,
haka muka kasance a gabanka, ya UBANGIJI.
18 Muna da ciki, mun yi ta murɗewa saboda zafi,
amma mun haifi iska.
Ba mu kawo ceto ga duniya ba;
ba mu haifi mutanen duniya ba.

19 Amma matattunka za su rayu;
jikunansu za su tashi.
Ku da kuke zama a ƙura,
ku farka ku kuma yi sowa don farin ciki.
Raɓarka kamar raɓar safiya ce;
duniya za tă haifi matattunta.

20 Ku tafi, mutanena, ku shiga ɗakunanku
ku kuma kulle ƙofofi;
ku ɓoye kanku na ɗan lokaci
sai ya huce fushinsa.
21 Duba, UBANGIJI yana fitowa daga mazauninsa
don yă hukunta mutanen duniya saboda zunubansu.
Duniya za tă bayyana zub da jinin da aka yi a kanta;
ba za tă ƙara ɓoye waɗanda aka kashe a cikinta ba.

# 27

*Ceton Isra'ila*

1 A wannan rana,
UBANGIJI zai yi hukunci da takobi,
takobinsa mai tsanani, mai ƙarfi da kuma mai muguwar ɓarna,
zai hukunta dodon ruwa macijin nan da ya kanannaɗe,
dodon ruwa macijin nan mai murɗewa;
zai kashe dodon nan na teku.
2 A wannan rana,
"Ku rera game da gonar inabi mai ba da 'ya'ya ku ce
3 Ni, UBANGIJI na lura da ita;
na yi ta yin mata banruwa.
Na yi tsaronta dare da rana
don kada wani yă yi mata ɓarna.
4 Ban yi fushi ba.
Da a ce ƙayayyuwa da sarƙaƙƙiya ne suke kalubalanta na mana!
Zan fita in yi yaƙi da su;
da na sa musu wuta duka.
5 Ko kuma bari su zo wurina don mafaka;
bari su yi sulhu da ni,
I, bari su yi sulhu da ni."

6 A kwanaki masu zuwa Yaƙub zai yi saiwa,

† **26:16** Ma'anar wannan kalma a Ibraniyanci don wannan jumla babu tabbas.

Isra'ila zai yi toho ya kuma yi fure
ya cika dukan duniya da 'ya'ya.

7 UBANGIJI ya buge shi
kamar yadda ya bugi waɗanda suka buge shi?
An kashe shi
kamar yadda aka kashe waɗanda suka kashe shi?
8 Ta wurin yaƙi da zaman bauta ka hukunta shi,
da tsananin tsawa kuma ka kore shi,
kamar a ranar da iskar gabas ta hura.
9 A ta haka fa, za a yi kafarar laifin Yaƙub,
wannan kuma zai zama cikakken amfanin kau da zunubinsa.
Sa'ad da ya niƙa duwatsun bagade
suka zama kamar allin da aka farfashe kucu-kucu,
har ba sauran ginshiƙan Ashera ko bagadan ƙona turare
da za a bari a tsaye.
10 Birni mai katanga ya zama kufai,
yasasshen mazauni, an yashe shi kamar hamada;
a can 'yan maruƙa suke kiwo,
a can suke kwance;
sun kakkaɓe rassanta ƙaf.
11 Sa'ad da rassanta suka bushe, sai su kakkarye su
mata kuma su zo su yi itacen wuta da su.
Gama mutane ne marar azanci;
saboda haka Mahaliccinsu bai ji tausayinsu ba,
Mahaliccinsu bai nuna musu jinƙai ba.

12 A wannan rana UBANGIJI zai tankaɗe daga Yuferites* mai gudu zuwa Rafin Masar,
ku kuma, ya Isra'ilawa, za a tattara ku ɗaya-ɗaya. 13 Kuma a wannan rana zai busa
ƙaho mai kāra sosai. Waɗanda suke mutuwa a Assuriya da kuma waɗanda aka kai
zaman bauta a Masar za su zo su kuma yi wa UBANGIJI sujada a dutse mai tsarki a
Urushalima.

# 28

*Kaiton Efraim*

1 Kaito ga wannan rawani, girman kai na mashayan Efraim,
ga fure mai yanƙwanewa, darajar kyansa,
da aka sa a kan kwari mai ba da amfani,
ga birnin nan, wadda take girman kan waɗanda aka ƙasƙantar da ruwan inabinsu!
2 Duba, Ubangiji yana da wanda yake da iko da kuma ƙarfi.
Kamar dutsen ƙanƙara da kuma iska mai ɓarna,
kamar kwararowar ruwa da rigyawa mai kirmewa,
zai jefa shi har ƙasa da ƙarfi.
3 Za a tattaka wannan rawani,
girman kai na mashayan Efraim da ƙafa.
4 Wannan fure mai yanƙwanewa, darajarar kyansa,
da aka sa a kan kwari mai ba da amfani,
zai zama kamar 'ya'yan ɓaure, nunan fari,
da zarar wani ya gani ya kuma tsinka,
zai haɗiye shi.

* 27:12 Da Ibraniyanci Kogi

5 A wannan rana UBANGIJI Maɗaukaki
zai zama rawani mai daraja
kyakkyawan rawani
wa mutanensa da suka ragu.
6 Zai zama ruhun adalci
gare shi wanda yake zaune a kujerar shari'a,
wurin samun ƙarfi
ga waɗanda suka kori abokan gāban da suka fāɗa musu da yaƙi a ƙofofi.

7 Da waɗannan kuma masu tangaɗi saboda sun sha ruwan inabi
suke jiri don sun sha barasa
Firistoci da annabawa suna tangaɗi saboda sun sha barasa
sun kuma yi tatur da ruwan inabi;
suna jiri saboda sun sha barasa,
suna tangaɗi sa'ad da suke ganin wahayi,
suna tuntuɓe sa'ad da suke ba da shawara.
8 Duk amai ya rufe teburori
kuma babu wani wurin da ba a ɓata ba.

9 "Wane ne yake so ya koyar?
Ga wa yake bayyana saƙonsa?
Ga yaran da aka yaye,
ga waɗanda ba a daɗe da yayewa ba ne?
10 Gama haka yake.
Yi ka kuma yi, yi ka kuma yi,
mulki a kan mulki, mulki a kan mulki;*
nan kaɗan, can kaɗan."

11 To da kyau, da leɓunan baƙi da ku harsunan da ba sani ba
Allah zai yi magana da wannan mutane,
12 waɗanda zai ce,
"Wannan shi ne wurin hutu, bari waɗanda suka gaji su huta";
da kuma, "Wannan shi ne wurin wartsakewa"
amma sun ƙi su saurara.
13 Saboda haka fa, maganar UBANGIJI gare su za tă zama,
Yi ka kuma yi, yi ka kuma yi,
mulki akan mulki, mulki a kan mulki;
nan kaɗan, can kaɗan,
domin su tafi su kuma fāɗi da baya,
su ji rauni a kuma kama su da tarko, a kai su zaman bauta.

14 Saboda haka ku saurari maganar UBANGIJI, ku masu ba'a
ku da kuke mulkin wannan mutane a Urushalima.
15 Kuna fariya cewa, "Mun yi alkawari da mutuwa,
mun kuma yi yarjejjeniya da kabari.
Sa'ad da zafi ya ratsa,
ba zai taɓa mu ba,
gama mun mai da ƙarya mafakarmu†
ruɗu kuma wurin ɓuyanmu."

* **28:10** Da Ibraniyanci / sab lasab sab lasab / kab lakab kab lakab (mai yiwuwa kalmomi marasa ma'ana ne; mai yiwuwa kwaikwayon maganar annabi ne); haka ma a aya 13. † **28:15** Ko kuwa allolin ƙarya

16 Saboda haka ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka ya ce,
"Duba, na kafa dutse a Sihiyona,
dutsen da aka gwada,
dutsen kusurwa mai daraja don tabbataccen tushe;
wanda ya dogara gare shi ba zai taɓa shan kunya ba.
17 Zan mai da gaskiya igiyar gwaji
adalci kuma ɗan katakon gwajin ginin;
ƙanƙara za tă share mafakarku,
ƙarya, da ruwa kuma za su mamaye maɓuyanku.
18 Za a soke alkawarinku da mutuwa;
yarjejjeniyarku da kabari ba zai zaunu ba.
Sa'ad da zafi mai ɓarna ya ratsa,
zai hallaka ku.
19 A duk sa'ad da ya zo;
ko da safiya, ko dare ko kuma da rana,
zai yi ta ratsawa yana kwasanku."

Za ku zama kamar mutumin
da ya zama abin karin magana,
20 wanda ya yi ƙoƙari yă kwanta a gajeren gado,
yă kuma rufa da ɗan siririn bargo.
21 UBANGIJI zai tashi kamar yadda ya yi a Dutsen Feratsim,
zai tā da kansa kamar a Kwarin Gibeyon
don yă aikata aikinsa, aikinsa da ba a saba gani ba,
yă kuma yi aikinsa, baƙon aikinsa.
22 Yanzu ku daina ba'arku,
in ba haka ba sarƙoƙinku za su ƙara nauyi;
Ubangiji, UBANGIJI Maɗaukaki, ya faɗa mini
game da hallakar da aka ƙaddara a kan dukan ƙasar.

23 Ku saurara ku kuma ji muryata;
ku kasa kunne ku kuma ji abin da na faɗa.
24 Sa'ad da manomi ya yi noma don shuki, yakan ci gaba da noma ne?
Yakan ci gaba da sara yana yin kunyoyi a ƙasa ne?
25 Sa'ad da ya shirya wuri da kyau,
ba yakan shuka kanumfari ya kuma yayyafa ɗaɗɗoya ba?
Ba yakan shuka alkama a kunyoyinsa‡
sha'ir a kunyoyinsa,§
tamba kuma a filinsa ba?
26 Allahnsa ya umarce shi
ya kuma koya masa hanyar da take daidai.

27 Ba a bugan kanumfari da ƙaton sanda
ko a yi ta jujjuye ƙafar keke a kan ɗaɗɗoya;
akan buga kanumfari da siririn sanda
ɗaɗɗoya kuma da tsumagiya.
28 Dole a niƙa hatsi don a yi burodi;
saboda haka mutum ba zai yi ta bugun alkama, har yă ɓata tsabar ba.
Ya san yadda zai sussuke alkamarsa,

‡ **28:25** Ba a tabbatar da ma'anar Ibraniyanci na wannan kalma ba. § **28:25** Ba a tabbatar da ma'anar Ibraniyanci na wannan kalma ba.

ba tare da ya ɓata tsabarta ba.
29 Dukan wannan hikimar takan zo daga UBANGIJI Maɗaukaki ne,
shi da yake mashawarci mai banmamaki, mafifici kuma cikin hikima.

# 29

*Kaiton birnin Dawuda*

1 Kaitonki, Ariyel,* Ariyel
birnin da Dawuda ya zauna!
Kara shekara ga shekara
a kuma bar shagulgulanki su yi ta kewayewa.
2 Duk da haka zan yi wa Ariyel kwanto
za tă kuma yi kuka da makoki,
za tă zama mini kamar bagaden jini.†
3 Zan kafa sansani kewaye da ke duka;
zan kewaye ki da hasumiyoyi
in tasar miki da ayyukan kwantona na yaƙi.
4 Za a ƙasƙantar da ke, za ki ƙi yin magana daga ƙasa;
maganarki za tă yi ƙasa-ƙasa daga ƙura.
Muryarki za tă zama kamar fatalwa daga ƙasa;
daga ƙura maganarki zai fito ƙasa-ƙasa.

5 Amma abokan gābanki masu yawa za su zama kamar ƙura mai laushi,
sojojinsu masu firgitarwa za su yi ta tashi kamar yayin da iska ta hura.
Farat ɗaya, cikin ɗan lokaci,
6 UBANGIJI Maɗaukaki zai zo
da tsawa da rawar ƙasa da ƙara mai girma,
da hadarin iska da guguwa da harshe na wuta mai ci.
7 Sa'an nan sojojin dukan al'umman da suka yi yaƙi da Ariyel,
da suka fāɗa mata da kagararta suka kuma yi mata kwanto,
za su zama kamar yadda yake da mafarki,
wahayi da dare,
8 kamar sa'ad da mai yunwa yana mafarki cewa yana cin abinci,
amma sai ya farka, yunwan tana nan;
kamar sa'ad da mai ƙishirwa yana mafarki cewa yana shan ruwa,
amma sai ya farka yana suma, da ƙishinsa.
Haka zai zama da sojoji na dukan al'ummai
da suka yi yaƙi da Dutsen Sihiyona.

9 Ku firgita ku kuma yi mamaki,
ku makance kanku ku kuma zama a makance;
ku bugu, amma ba da ruwan inabi ba,
ku yi tangaɗi, amma ba daga barasa ba.
10 UBANGIJI ya kawo muku barci mai nauyi,
Ya rufe idanunku (annabawa);
ya rufe kawunanku (masu duba).
11 Gare ku duk wannan wahayi ba kome ba ne sai dai maganganun da aka rufe a
cikin littafi. In kuma kun ba da littafin ga wani wanda zai iya karanta, kuka kuma

* **29:1** Ariyel. Wata ma'ana mai yiwuwa ta "ariyel" a Ibraniyanci za tă iya zama "Jarumi na Allah" ko kuwa "Zaki na Allah" ko kuma "Bagade na Allah." † **29:2** Ibraniyanci na bagaden jini ya yi kamar Ibraniyanci na Ariyel.

ce masa, “Karanta wannan, muna roƙonka,” zai amsa ya ce, “Ba zan iya ba; an rufe
shi.” 12 Ko kuwa in kun ba da littafin ga wani wanda ba zai iya karantawa ba, kuka
kuma ce, “Karanta wannan, muna roƙonka,” zai amsa ya ce, “Ban iya karatu ba.”
13 Ubangiji ya ce,

“Waɗannan mutane sun zo kusa da ni da bakinsu
suka kuma girmama ni da leɓunansu,
amma zukatansu suna nesa daga gare ni.
Sujadar da suke mini
cike take da dokokin da mutane suka koyar.‡
14 Saboda haka zan firgita waɗannan mutane sau ɗaya
da abubuwan banmamaki a kan abubuwan banmamaki;
hikimar masu hikima za tă lalace,
azancin masu azanci zai ɓace.”
15 Kaiton waɗanda suke zuwa manyan zurfafa
don su ɓoye shirye-shiryensu daga Ubangiji,
waɗanda suke aikinsu cikin duhu su yi tunani,
“Wa yake ganinmu? Wa zai sani?”
16 Kuna birkitar abubuwa,
sai ka ce an mayar da mai ginin tukwane ya zama yumɓu!
Abin da aka yi zai ce wa wanda ya yi shi,
“Ba shi ne ya yi ni ba”?
Tukunya za tă iya ce wa mai ginin tukwane,
“Ba ka san kome ba”?

17 Cikin ɗan lokaci, za a mai da Lebanon gona mai taƙi
kuma gona mai taƙi za tă zama kamar kurmi?
18 A wannan rana kurame za su ji maganganun littafi,
daga duruduru da duhu kuma
idanun makafi za su gani.
19 Masu tawali’u za su sāke yin farin ciki a cikin Ubangiji;
mabukata za su yi farin ciki cikin Mai Tsarkin nan na Isra’ila.
20 Masu zalunci za su ƙare,
masu ba’a za su ɓace,
kuma dukan waɗanda suke da ido don mugunta za su hallaka,
21 waɗanda ta magana kawai sukan mai da mutum mai laifi,
waɗanda suke kafa tarko wa mai ba da kāriya a ɗakin shari’a
da shaidar ƙarya kuma su hana marar laifi samun shari’ar adalci.
22 Saboda haka ga abin da Ubangiji wanda ya fanshi Ibrahim, ya ce wa gidan Yaƙub,

“Ba za a ƙara kunyata Yaƙub ba;
fuskokinsu kuma ba za su ƙara yanƙwanewa ba.
23 Sa’ad da suka ga ’ya’yansu a tsakiyarsu,
aikin hannuwansu,
za su kiyaye sunana da tsarki;
za su san tsarkin Mai Tsarkin nan na Yaƙub,
za su kuma ji tsoron Allah na Isra’ila.
24 Su da suke marasa azanci a ruhu za su sami fahimtar;
waɗanda suke gunaguni za su yarda da koyarwa.”

‡ **29:13** Da Ibraniyanci; Seftuwajin Suna mini sujada a banza; koyarwarsu ba kome ba ne illa dokokin da mutane suka koyar

# 30

*Kaiton al'umma mai tayarwa*

1 "Kaiton 'ya'ya masu tayarwa,"
in ji UBANGIJI,
"ga waɗanda suke ƙulle-ƙullen da ba nawa ba,
suna yin yarjejjeniya, amma ba ta Ruhuna ba,
suna jibga zunubi a kan zunubi;
2 waɗanda suka gangara zuwa Masar
ba tare da sun nemi shawarata;
waɗanda suke neman taimakon kāriyar Fir'auna,
don neman inuwar mafakar Masar.
3 Amma kāriyar Fir'auna za tă zama muku abin kunya,
inuwar Masar za tă jawo muku kunya.
4 Ko da yake suna da shugabanni a Zowan
kuma jakadunsu sun iso Hanes,
5 kowa zai sha kunya
saboda mutanen da ba su da amfani gare su,
waɗanda ba sa taimako ko amfani,
sai dai jawo kunya da da-na-sani."
6 Allah ya faɗa game da dabbobin Negeb cewa,
Ta cikin ƙasa mai wahala da mai hatsari
inda zakoki da zakanya,
inda macizai masu dafi da macizai masu tashi sama suke,
jakadu na ɗaukan arzikinsu a kan jakuna,
dukiyarsu a kan raƙuma,
zuwa ƙasan nan marar riba,
7 zuwa Masar, wadda taimakonta marar amfani ne.
Saboda haka na yi mata laƙabi
Rahab Marar Yin Kome.

8 Tafi yanzu, ka rubuta musu a kan allo,
ka rubuta shi a kan littafi,
cewa kwanaki suna zuwa
zai zama madawwamin shaida.
9 Waɗannan mutane masu tawaye, 'ya'ya masu ruɗu,
'ya'yan da ba sa niyya su saurara ga umarnan UBANGIJI.
10 Sukan ce wa masu gani,
"Kada ku ƙara ganin wahayi!"
Ga annabawa kuwa sukan ce,
"Kada ku ƙara ba mu wahayin abin da yake daidai!
Faɗa mana abubuwan da muke so mu ji ne kawai,
ku yi annabcin abin da zai ruɗe mu.
11 Ku bar wannan hanya,
ku tashi daga wannan hanya,
ku kuma daina kalubalantarmu
da Mai Tsarkin nan na Isra'ila!"
12 Saboda haka, ga abin da Mai Tsarkin nan na Isra'ila yake cewa,
"Saboda haka kun ƙi wannan saƙo,
kuka dogara ga aikin kama-karya
kuka kuma dogara ga yin ruɗu,
13 wannan zunubi zai zama muku
kamar bango mai tsayi, tsagagge da yake kuma fāɗuwa,

da zai rushe nan da nan, ba tsammani.
14 Zai rushe kucu-kucu kamar tukunyar yumɓu,
ya ragargaje ƙaf
har cikin gutsattsarinsa ba za a sami ko ɗan katanga
don ɗiba garwashin wuta
ko a ɗiba ruwa daga tanki ba."
15 Ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka, Mai Tsarkin nan na Isra'ila ya faɗa,
"Cikin tuba da hutu ne kaɗai cetonku yake,
cikin shiru da dogara gare ni ne za ku sami ƙarfinku,
amma ba za ku sami ko ɗaya a cikinsu ba.
16 Kun ce, 'A'a, za mu gudu a kan dawakai.'
Saboda haka za ku gudu!
Kun ce, 'Za mu hau dawakai masu sauri mu gudu.'
Saboda haka masu fafararku za su fi ku gudu!
17 Dubu za su gudu
don barazanar mutum guda;
da jin barazanar mutane biyar
dukanku za ku yi ta gudu
sai an bar ku
kamar sandar tuta a kan dutse,
kamar tuta a kan tudu."

18 Duk da haka UBANGIJI yana marmari ya yi muku alheri;
ya tashi don yǎ nuna muku jinƙai.
Gama UBANGIJI Allah ne mai aikata gaskiya.
Masu albarka ne dukanku waɗanda suke dogara gare shi!
19 Ya mutanen Sihiyona, waɗanda suke zama a Urushalima, ba za ku ƙara kuka
ba. Zai zama mai alheri sa'ad da kuka yi kukan neman taimako! Da zarar ya ji, zai
amsa muku. 20 Ko da yake Ubangiji yakan ba da abincin azaba da ruwan wahala, ba
za a ƙara ɓoye malamanku ba; da idanunku za ku gan su. 21 Ko kun juye dama ko
hagu, kunnuwanku za su ji murya a bayanku tana cewa, "Ga hanya; ku yi tafiya a
kai." 22 Sa'an nan za ku ƙazantar da gumakanku da kuka dalaye da zinariya; za ku
zubar da su kamar rigar al'adar mace ku kuma ce musu, "Ku ɓace mana da gani!"
23 Zai kuma aiko muku da ruwan sama don shuki a ƙasa, kuma abincin da zai fito
daga gona zai zama mai albarka da kuma mai yawa. A wannan rana shanu za su yi
kiwo a wadatacciyar makiyaya. 24 Shanunku da jakunanku da suke huɗar gonakinku
za su ci harawa mafi kyau, wanda an sheƙe shi da babban cokali mai yatsu da kuma
babban cokali. 25 A ranar babban kisa, sa'ad da hasumiyoyi za su fāɗi, rafuffukan
ruwa za su malalo a kan kowane dutse da kowane tudu mai tsawo. 26 Wata zai yi
haske kamar rana, kuma hasken rana zai ma yi sau bakwai na haskenta, kamar
hasken cikakku ranaku bakwai, sa'ad da UBANGIJI zai ɗaura raunukan mutanensa ya
kuma warkar da raunukan da ya yi musu.
27 Duba, Sunan UBANGIJI yana zuwa daga nesa,
tare da fushi mai ƙuna da kuma baƙin hayaƙi;
leɓunansa sun cika da fushi,
harshensa kuma wuta ce mai cinyewa.
28 Numfashinsa kamar raƙuman ruwa masu gudu
yana tashi har zuwa wuya.
Yakan tankaɗe al'ummai cikin lariyar hallaka;
yakan sa a muƙamuƙan mutane
linzamin da zai jagorance su su kauce.

29 Za ku kuma rera
kamar a daren da kuke shagalin biki mai tsarki;
zukatanku za su yi farin ciki
kamar sa'ad da mutane sukan haura da busa
zuwa dutsen UBANGIJI,
zuwa Dutse na Isra'ila.
30 UBANGIJI zai sa mutane su ji muryarsa mai daraja
ya kuma sa su ga hannunsa na saukowa
tare da fushi mai ƙuna da kuma wuta mai cinyewa,
gizagizai za su ɓarke, za a yi hadarin tsawa da ƙanƙara.
31 Muryar UBANGIJI za tă firgita Assuriya
da sandar mulkinsa zai kashe su.
32 Kowane bugun da UBANGIJI zai yi musu
da bulalarsa na hukunci
zai zama kiɗi ga ganguna da garaya,
yayinda yake yaƙi da su da naushin hannunsa.
33 An riga an shirya wurin ƙonawa;
an shirya shi saboda sarki.
An haƙa ramin wutarsa da zurfi da kuma fāɗi,
da isashen wuta da itacen wuta;
numfashin UBANGIJI,
yana kamar kibiritu mai ƙuna,
da aka sa masa wuta.

# 31

*Kaiton waɗanda suke dogara ga Masar*

1 Kaiton waɗanda suka gangara zuwa Masar don neman taimako,
waɗanda suke dogara ga dawakai,
waɗanda suke dogara ga yawan kekunan yaƙinsu
da kuma a girman ƙarfin mahayan dawakansu,
amma ba sa dogara ga Mai Tsarkin nan na Isra'ila,
ko ya nemi taimako daga UBANGIJI.
2 Shi ma yana da hikima kuma zai iya kawo masifa;
ba ya janye kalmominsa.
Zai yi gāba da gidan mugu,
gāba da waɗanda suke taimakon masu aikata mugunta.
3 Amma Masarawa mutane ne ba Allah ba;
dawakansu nama da jini ne ba ruhu ba.
Sa'ad da UBANGIJI ya miƙa hannunsa,
shi da yake taimako zai yi tuntuɓe
shi da aka taimaka zai fāɗi;
dukansu biyu za su hallaka tare.
4 Ga abin da UBANGIJI ya faɗa mini,
"Kamar yadda zaki kan yi ruri
babban zaki a kan abin da ya yi farauta,
kuma ko da yake dukan ƙungiyar makiyaya
sun taru wuri ɗaya a kansa,
ba zai jijjigu ta wurin ihunsu ba
ko ya damu da kiraye-kirayensu,
ta haka UBANGIJI Maɗaukaki zai sauko
don yă yi yaƙi a kan Dutsen Sihiyona da kuma a kan ƙwanƙolinsa.

5 Kamar tsuntsaye masu shawagi a sama
haka UBANGIJI Maɗaukaki zai kiyaye Urushalima;
zai kāre ta ya kuma fanshe ta,
zai 'ƙetare' ta ya kuma kuɓutar da ita."
6 Ku dawo gare shi ku da kuka yi masa babban tayarwa, ya Isra'ilawa. 7 Gama a
wannan rana kowannenku zai ƙi gumakan azurfa da zinariya da hannuwanku masu
zunubi suka yi.
8 "Za a karkashe Assuriyawa da takobin da ba na yin mutum ba;
takobi, da ba na yin mutum ba, zai cinye.
Za su gudu daga takobi
za a kuma sa samarinsu aikin dole.
9 Kagarарsu za tă fāɗi saboda razana;
da ganin matsayin yaƙin, shugabannin yaƙinsu za su firgita,"
in ji UBANGIJI,
wanda wutarsa tana a Sihiyona,
wanda matoyarsa tana a Urushalima.

## 32

*Mulkin adalci*
1 Duba, sarki zai yi mulki cikin adalci
masu mulki kuma su yi mulki da adalci.
2 Kowane mutum zai zama kamar wurin fakewa daga iska
mafaka kuma daga hadari,
kamar rafuffukan ruwa a hamada
da kuma inuwar babban dutse a ƙeƙasasshiyar ƙasa.
3 Sa'an nan idanun waɗanda suka gani ba za su ƙara rufewa ba,
kunnuwan waɗanda suka ji kuma za su saurara.
4 Zuciya marasa haƙuri za su sani su kuma fahimta,
harshen masu ana'ana kuma zai sāke su yi magana sosai.
5 Ba za a ƙara ce da wawa mai girma ba
ko kuwa a ɗaukaka mazambaci.
6 Gama wawa maganar wauta yakan yi,
zuciyarsa ta cika da mugunta,
yana aikata abubuwan rashin sanin Allah
yana baza kurakurai game da UBANGIJI;
yana barin mayunwata da yunwa
ya kuma hana masu ƙishirwa ruwan sha.
7 Matakan mazambaci mugaye ne,
yana ƙulla mugayen shirye-shirye
don yă hallaka talakawa da ƙarairayi,
ko sa'ad da roƙon mai bukata da gaskiya ne.
8 Amma mutumin kirki kan yi shirye-shirye masu kirki,
kuma yakan tsaya a kan ayyukan kirki.

*Matan Urushalima*
9 Ku matan da kuke zaman jin daɗi,
ku tashi ku saurare ni;
ku 'yan matan da kuke tsammani kuna da kāriya,
ku ji abin da zan faɗa!
10 Cikin ɗan lokaci ƙasa da shekara guda
ku da kuke tsammani kuna da kāriya za ku yi rawar jiki;

girbin ʼyaʼyan inabi zai kāsa,
girbin ʼyaʼyan itatuwa kuma ba zai zo ba.
11 Ku yi rawar jiki, ku mata masu jin daɗi,
ku sha wahala, ku ʼyan matan da kuke tsammani kuna da kāriya!
Ku tuɓe rigunanku,
ku ɗaura tsummoki a kwankwasonku.
12 Ku bugi ƙirjinku don gonaki masu kyau
don ʼyaʼyan inabi
13 da kuma don ƙasar mutanena,
da ƙasar da ƙayayyuwa da sarƙaƙƙiya ne suka yi girma,
I, ku yi kuka saboda dukan gidajen da dā ake biki
da kuma domin wannan birnin da dā ake murna a ciki.
14 Za a ƙyale kagarar,
a gudu a bar birnin da dā ake hayaniya;
mafaka da hasumiyar tsaro za su zama kango har abada,
jin daɗin jakuna, makiyaya don garkuna,
15 sai an zubo Ruhu a kanmu daga sama,
hamada kuma ta zama ƙasar mai taƙi,
gona mai taƙi kuma ta zama kamar kurmi.
16 Aikin gaskiya zai zauna a hamada
adalci kuma zai zauna a ƙasa mai taƙi.
17 Aikin adalci zai zama salama;
tasirin adalci zai zama natsuwa da tabbaci har abada.
18 Mutanena za su zauna lafiya a wuraren salama,
a gidaje masu kāriya,
a wuraren hutun da babu fitina.
19 Ko da yake ƙanƙara za tă fāɗo a jeji,
a kuma rurrushe birni gaba ɗaya,
20 zai zama muku da albarka,
ku da kuke shuki iri kusa da kowane rafi,
kuna kuma barin lafiyayyiyar makiyaya domin shanu da jakunanku.

# 33

*Damuwa da taimako*

1 Kaitonka, ya kai mai hallakarwa,
kai da ba a hallakar da kai ba!
Kaitonka, ya maciya amana,
kai da ba a ci amanarka ba!
Saʼad da ka daina hallakarwa,
za a hallaka ka;
saʼad da ka daina cin amana,
za a ci amanarka.
2 Ya UBANGIJI, ka yi mana jinƙai;
muna marmarinka.
Ka zama ƙarfinmu kowace safiya,
cetonmu a lokacin damuwa.
3 Da tsawar muryarka, mutane za su gudu;
saʼad da ka tashi, alʼummai za su watse.
4 Ganimarku, ya alʼummai ƙanana fāri sun girbe;
kamar tarin fārin da mutane sun fāɗa wa.

5 UBANGIJI da girma yake, gama yana zaune a bisa;
zai cika Sihiyona cikin gaskiya da adalci.

6 Zai zama tabbataccen harsashi na koyaushe,
ma'ajin ceto da hikima da sani a yalwace;
tsoron UBANGIJI shi ne mabuɗin wannan dukiya.*

7 Duba, jarumawansu suna kuka da ƙarfi a tituna;
jakadun salama suna kuka mai zafi.
8 An gudu an bar manyan hanyoyi,
babu matafiye a kan hanyoyi.
Aka keta yarjejjeniya,
an rena shaidunsa
ba a kuwa ganin girman kowa.
9 Kasa tana kuka an kuma gudu an bar ta,
Lebanon ta sha kunya ta kuma yanƙwane;
Sharon ta zama kamar Araba,
Bashan da Karmel sun kakkaɓe ganyayensu.

10 "Yanzu zan tashi," in ji UBANGIJI.
"Yanzu ne za a ɗaukaka ni;
yanzu za a ɗaga ni sama.
11 Kun yi cikin yayi,
kuka haifi kara;
numfashinku wuta ne da zai cinye ku.
12 Za a ƙone mutane kamar da ƙuna farar ƙasa;
kamar ƙayayyuwan da aka sare aka kuma sa musu wuta."

13 Ku da kuke da nesa, ku ji abin da na yi;
ku da kuke kusa, ku san ikona!
14 Masu zunubi a Sihiyona sun firgita;
rawar jiki ya kama marasa sanin Allah suna cewa,
"Wane ne a cikinmu zai iya zama da wuta mai ci?
Wane ne a cikinmu zai iya zama da madawwamiyar ƙonewa?"
15 Shi da yake tafiya cikin adalci
yana kuma magana abin da yake daidai,
wanda yake ƙin riba daga cuta
yana kuma kiyaye hannunsa daga karɓan cin hanci,
wanda yake hana kunnuwansa daga ƙulla kisa
ya kuma rufe idanunsa a kan tunanin aikata mugunta,
16 shi ne mutumin da zai zauna a bisa,
wanda mafakarsa za tă zama kagarar dutse.
Za a tanada abincinsa, kuma ruwa ba zai kāsa masa ba.

17 Idanunku za su ga sarki a cikin kyansa
ku kuma hangi ƙasar da take shimfiɗe can da nisa.
18 Cikin tunaninku za ku yi tunani firgitar da ta faru tun dā kuna cewa,
"Ina hafsan nan?
Ina wannan wanda yake karɓar haraji?
Ina hafsan da yake lura da hasumiyoyi?"
19 Ba za ku ƙara ganin waɗannan mutane masu girman kai kuma ba,
waɗannan mutane masu magana da harshen da ba ku fahimta ba.

* **33:6** Ko kuwa dukiya ce daga wurinsa

20 Ku duba Sihiyona, birnin shagulgulanmu;
idanunku za su ga Urushalima,
mazauni mai lafiya, tentin da ba za a taɓa gusar ba;
wanda ba a taɓa tumɓuke turakunsa ba,
ko a tsinke igiyoyinta.
21 A can UBANGIJI zai zama Mai Iko Duka namu.
Zai zama kamar inda manyan koguna da rafuffuka suke.
Matuƙan jirgin ruwa ba za su kai wurinsu ba,
manyan jiragen ruwa ba za su yi zirga-zirga a kansu ba.
22 Gama UBANGIJI ne alƙalinmu,
UBANGIJI ne mai ba mu dokoki,
UBANGIJI ne sarkinmu;
shi ne wanda zai cece mu.

23 Maɗaurinku sun kunce
ƙarfafan itacen jirgin ba su da kāriya,
fikafikan jirgin ba su buɗu ba.
Ta haka za a raba yalwar ganima
har ma guragu za su kwashe ganimar.
24 Ba wani mazauna a Sihiyona da zai ce, "Ina ciwo";
za a kuma gafarta zunuban waɗanda suke zama a can.

# 34

*Hukunci a kan al'ummai*

1 Ku zo kusa, ku al'ummai, ku kuwa saurara
ku kasa kunne, ku mutane!
Bari duniya ta ji, da kuma dukan abin da yake cikinta,
duniya, da dukan abin da yake fitowa daga gare ta!
2 UBANGIJI yana fushi da dukan al'ummai;
hasalarsa tana a kan mayaƙansu.
Zai hallaka su tas,
zai ba da su a karkashe.
3 Za a jefar da waɗanda aka kashe
gawawwakinsu za su yi wari;
duwatsu za su jiƙu da jininsu.
4 Za a tumɓuke dukan taurarin sammai
za a kuma nannaɗe sararin sama kamar littafi;
dukan rundunar sama za su fāffāɗi
kamar ganyayen da suka yanƙwane daga kuringa,
kamar 'ya'yan ɓauren da suka bushe daga itacen ɓaure.
5 Takobina ya sha zararsa a cikin sammai;
duba, ya sauko cikin hukunci a kan Edom,
mutanen da zan hallaka tas.
6 Takobin UBANGIJI ya jiƙu da jini,
ya rufu da kitse,
jinin raguna da na awaki,
kitse daga ƙodar raguna.
Gama UBANGIJI ya yi hadayar Bozra
da kuma babban kisa a Edom.
7 Babban bijimin jeji zai fāɗi tare da su,
maruƙan bijimi da manyan bijimai.
Kasarsu za tă cika da jini,

ƙura kuma zai cika da kitse.

8 Gama UBANGIJI yana da ranar ɗaukar fansa,
shekarar ramuwa, don biya wa Sihiyona bukata.
9 Za a mai da rafuffukan Edom rami,
ƙurarta za tă zama kibiritun farar wuta;
ƙasarta za tă zama rami mai ƙuna!
10 Ba za a kashe ta ba dare da rana;
hayaƙinta za tă yi ta tashi har abada.
Daga tsara zuwa tsara za tă zama kango;
babu wani da zai ƙara wucewa ta wurin.
11 Mujiyar hamada da mujiya mai kuka za su mallake ta;
babban mujiya da hankaka za su yi sheƙa a can.
Allah zai miƙe a kan Edom
magwajin bala'i
da ma'aunin kango.
12 Sarakunanta ba za su kasance da wani abin da ake kira masarauta ba,
dukan sarakunanta za su ɓace.
13 Kayayuwa za su mamaye fadodinta
ƙayayyuwa da sarƙaƙƙiya za su cika kagaranta.
Za tă zama mazaunin diloli
da gida don mujiyoyi.
14 Halittun hamada za su sadu da kuraye,
awakin jeji za su yi ta kiran juna;
a can halittun dare su ma za su huta
su kuma nemi wurin hutu wa kansu.
15 Mujiya za tă yi sheƙa a can ta zuba ƙwai;
za tă ƙyanƙyashe su, ta kuma kula da 'ya'yanta a inuwar fikafikanta;
a can kuma shirwa za su taru,
kowa da abokinsa.
16 Duba a cikin littafin UBANGIJI ka kuma karanta.
Babu wani a cikin waɗannan da ya ɓace,
babu ko ɗaya da ba ta da abokiya.
Gama bakinsa ne ya ba da umarni,
Ruhunsa kuma zai tara su wuri ɗaya.
17 Ya ba su rabonsu;
hannunsa ya rarraba musu ta wurin awo.
Za su mallake ta har abada
su kuma zauna a can daga tsara zuwa tsara.

# 35

*Farin cikin waɗanda aka ceta*

1 Hamada da ƙeƙasasshiyar ƙasa za su yi murna;
jeji zai yi farin ciki ya kuma hudo.
Kamar fure, 2 zai buɗu ya hudo;
zai yi farin ciki mai girma ya kuma yi sowa don farin ciki.
Za a maido wa Lebanon da darajarta,
darajar Karmel da Sharon;
za su ga ɗaukakar UBANGIJI,
darajar Allahnmu.
3 Ku ƙarfafa hannuwa marasa ƙarfi,
ku ƙarfafa gwiwoyin da suka gaji;

4 ku faɗa wa waɗanda suka karai a zukata,
“Ku yi ƙarfin hali, kada ku ji tsoro;
Allahnku zai zo,
zai zo domin ya ɗau fansa;
da ramuwar Allah
zai zo don yǎ cece ku.”

5 Sa’an nan idanun makafi za su buɗe
kunnuwan kurame kuma su ji.
6 Sa’an nan guragu za su yi tsalle kamar barewa,
bebaye kuma su yi sowa don farin ciki.
Ruwa zai kwararo daga jeji
rafuffuka kuma a cikin hamada.
7 Yashi mai ƙuna zai zama tafki,
ƙeƙasasshiyar ƙasa kuma za tǎ cika da maɓulɓulan rafuffuka.
A mazaunin diloli, inda suka taɓa zama,
ciyawa da iwa da kyauro za su yi girma.

8 Kuma babbar hanya za tǎ kasance a can;
za a ce ta ita Hanyar Mai Tsarki.
Marasa tsarki ba za su yi tafiya a kanta ba;
za tǎ zama domin waɗanda suka yi tafiya a wannan Hanya ce;
mugaye da wawaye ba za su yi ta yawo a kanta ba.
9 Zaki ba zai kasance a can ba,
balle wani naman jeji mai faɗa ya haura kanta;
ba za a same su a can ba.
Amma fansassu ne kaɗai za su yi tafiya a can,
10 kuma fansassu na Ubangiji za su komo.
Za su shiga Sihiyona da rerawa;
matuƙar farin ciki zai mamaye su.
Murna da farin ciki za su sha kansu,
baƙin ciki kuma da nishi za su gudu.

## 36

*Sennakerib ya yi wa Urushalima barazana*
*(2 Sarakuna 18.13-27; 2 Tarihi 32.1-19)*

1 A shekara ta goma sha huɗu ta mulkin Sarki Hezekiya, Sennakerib sarkin Assuriya
ya kai wa dukan birane masu kagaran Yahuda yaƙi ya kuma kame su. 2 Sai sarkin
Assuriya ya aiki sarkin yaƙinsa tare da mayaƙa masu yawa daga Lakish zuwa
wurin Sarki Hezekiya a Urushalima. Sa’ad da sarkin yaƙi ya tsaya a wuriyar Tafkin
Tudu, a hanya zuwa Filin Mai Wanki, 3 Eliyakim ɗan Hilkiya sarkin fada, Shebna
magatakarda, da Yowa ɗan Asaf marubuci suka fita zuwa wurinsa.
4 Sai sarkin yaƙin ya ce musu, “Ku faɗa wa Hezekiya.
“ ‘Ga abin da babban sarki, sarkin Assuriya, ya faɗa. A kan me kake dangana
wannan ƙarfin halinka? 5 Ka ce kana da dabara da kuma ƙarfin mayaƙa, amma
kana magana banza ce kawai. Ga wa ka dogara, da kake tayar mini? 6 Yanzu
duba, kana dogara ga Masar, wannan ɗan tsinken kyauron dogarawa, wanda zai
soki hannun mutum yǎ kuma ji masa rauni in ya dangana a kansa! Haka Fir’auna
sarkin Masar yake ga duk wanda ya dogara da shi. 7 Kuma in ka ce mini, “Mun
dogara ga Ubangiji Allahnmu ne” ba shi ba ne Hezekiya ya rurrushe masujadan

kan tudunsa da bagadansa, yana ce wa Yahuda da Urushalima, “Dole ku yi sujada
wa gaban wannan bagade”?
8 “ ‘Yanzu fa, bari in yi ciniki da maigidana, sarki Assuriya. Zan ba ka dawakai
dubu biyu, in za ka sa mahaya a kansu! 9 Yaya za ka ƙi hafsan mafi ƙanƙanci
na hafsoshin maigidana, ko da yake kana dogara ga Masar don kekunan yaƙi da
mahayan dawakai? 10 Ban da haka kuma, na zo ne in faɗa in kuma hallaka wannan
ƙasa ba tare da Ubangiji ba? Ubangiji kansa ya faɗa mini in tasar wa wannan ƙasa
in kuma hallaka ta.’ ”
11 Sai Eliyakim, Shebna da Yowa suka ce wa sarkin yaƙin, “Ka yi haƙuri ka yi wa
bayinka magana da Arameyanci, da yake muna jinsa. Kada ka yi mana magana da
Yahudanci a kunnen mutanen da suke kan katanga.”
12 Amma sarkin yaƙin ya amsa ya ce, “Kuna tsammani ga maigidanku da ku ne
kawai maigidana ya aiko ni in yi waɗannan maganganu, ba ga mutanen da suke zama
a kan katanga ba, waɗanda kamar ku, za su ci kashinsu su kuma sha fitsarinsu?”
13 Sa’an nan sarkin yaƙin ya tsaya ya kuma yi kira da Yahudanci ya ce, “Ku ji
kalmomin babban sarki, sarkin Assuriya! 14 Ga abin da sarki ya ce kada ku bar
Hezekiya ya ruɗe ku. Ba zai cece ku ba! 15 Kada ku bar Hezekiya ya rarashe ku ku
dogara ga Ubangiji sa’ad da ya ce, ‘Tabbatacce Ubangiji zai cece mu; ba za a ba da
wannan birni a hannun sarkin Assuriya ba.’
16 “Kada ku saurari Hezekiya. Ga abin da sarkin Assuriya ya faɗa. Ku nemi salama
da ni ku kuma fito zuwa wurina. Ta haka kowa zai ci daga kuringarsa da kuma itacen
ɓaurensa ya kuma sha ruwa daga tankinsa, 17 sai na zo na kuma kwashe ku zuwa
ƙasa kamar taku, ƙasar hatsi da kuma sabon ruwan inabi, ƙasar abinci da gonakin
inabi.
18 “Kada ku bar Hezekiya ya ruɗe ku sa’ad da ya ce, ‘Ubangiji zai cece mu.’ Allahn
wata al’umma ya taɓa ceci ƙasarsa daga hannun sarkin Assuriya? 19 Ina allolin
Hamat da na Arfad? Ina allolin Sefarfayim? Sun fanshi Samariya daga hannuna?
20 Wanne cikin dukan allolin ƙasashen nan ya iya ceton ƙasarsa daga gare ni? Yaya
kuwa Ubangiji zai iya ceci Urushalima daga hannuna?”
21 Amma mutanen suka yi shiru ba su kuwa ce kome ba, gama sarki ya yi umarni
cewa, “Kada ku amsa masa.”
22 Sai Eliyakim ɗan Hilkiya sarkin fada, Shebna magatakarda, da kuma Yowa ɗan
Asaf marubuci suka tafi wurin Hezekiya, da rigunansu a kyakkece, suka kuwa faɗa
masa abin da sarkin yaƙin ya yi ta farfaɗa.

# 37

*An yi faɗin ceton Urushalima*
*(2 Sarakuna 19.1-13)*

1 Sa’ad da Sarki Hezekiya ya ji haka, sai ya kyakkece rigunansa ya kuma sanya
tsummoki ya tafi ya shiga haikalin Ubangiji. 2 Ya aiki Eliyakim sarkin fada, Shebna
magatakarda da kuma manyan firistoci, duka sanye da tsummoki, wurin Ishaya ɗan
Amoz. 3 Suka faɗa masa cewa, “Ga abin da Hezekiya ya ce wannan rana ce ta
baƙin ciki da tsawatawa da shan kunya, sai ka ce sa’ad da ’ya’ya kan zo matakin
haihuwa sa’an nan a rasa ƙarfin haihuwarsu. 4 Mai yiwuwa Ubangiji Allahnka zai
ji maganganun sarkin yaƙin da maigidansa, sarkin Assuriya, ya aika don yǎ zagi
Allah mai rai, ya kuma tsawata masa saboda maganganun da Ubangiji Allahnka ya
ji. Saboda haka ka yi addu’a saboda raguwar da suke da rai.”
5 Sa’ad da shugabannin Sarki Hezekiya suka zo wurin Ishaya, 6 sai Ishaya ya ce
musu, “Ku faɗa wa maigidanku cewa, ‘Ga abin da Ubangiji ya faɗa. Kada ka ji
tsoron abin da ka ji, maganganun nan da bayin sarkin Assuriya suka yi mini saɓo.

7 Ka saurara! Zan sa ruhuna a cikinsa saboda sa’ad da ya ji wani labari, zai koma
zuwa ƙasarsa, a can kuwa zan sa a kashe shi da takobi.’ ”
8 Sa’ad da sarkin yaƙin ya ji cewa sarkin Assuriya ya bar Lakish, sai ya janye ya
kuma sami sarki yana yaƙi da Libna.
9 To, fa, Sennakerib ya sami labari cewa Tirhaka, mutumin Kush sarkin Masar,
yana fitowa don yă yi yaƙi da shi. Sa’ad da ya ji haka, sai ya aiki jakadu zuwa wurin
Hezekiya da wannan magana. 10 “Ku faɗa wa Hezekiya sarkin Yahuda cewa kada ka
bar allahn da ka dogara a kai ya ruɗe ka sa’ad da ya ce, ‘Ba za a ba da Urushalima
ga sarkin Assuriya ba.’ 11 Tabbatacce ka ji abin da sarakunan Assuriya suka aikata
ga dukan ƙasashe, suna hallaka su tas. Kai kuwa za ka tsira ne? 12 Allolin al’umman
da kakannina suka hallaka sun cece su ne, allolin Gozan, Haran, Rezef da kuma na
mutanen Eden waɗanda suke zama a Tel Assar? 13 Ina sarkin Hamat yake, sarkin
Arfad fa, sarkin Sefarfayim, ko na Hena ko na Iffa?”

### *Addu’ar Hezekiya*
### *(2 Sarakuna 19.14-19)*

14 Hezekiya ya karɓi wasiƙar daga jakadun ya karanta ta. Sa’an nan ya haura zuwa
haikalin UBANGIJI ya shimfiɗa ta a gaban UBANGIJI. 15 Sai Hezekiya ya yi addu’a ga
UBANGIJI ya ce, 16 “Ya UBANGIJI Allah Maɗaukaki, Allah na Isra’ila, zaune a tsakanin
kerubobi, kai kaɗai ne Allah a kan dukan masarautan duniya. 17 Ka kasa kunne, ya
UBANGIJI, ka kuma ji; ka buɗe idanunka, ya UBANGIJI, ka kuma gani; ka saurara ga
dukan maganganun da Sennakerib ya aika don yă zagi Allah mai rai.
18 “Gaskiya ce, ya UBANGIJI, cewa sarakunan Assuriyawa sun mai da dukan
waɗannan mutane da ƙasashensu kango. 19 Sun jefar da gumakansu cikin wuta
suka kuma hallaka su, gama su ba alloli ba ne itace ne kawai da dutse, da hannuwan
mutane suka sarrafa. 20 Yanzu, ya UBANGIJI Allahnmu, ka cece mu daga hannunsa,
saboda masarautai a duniya su san cewa kai kaɗai ne, ya UBANGIJI, Allah.”

### *Fāɗuwar Sennakerib*
### *(2 Sarakuna 19.20-34)*

21 Sa’an nan Ishaya ɗan Amoz ya aika da saƙo wa Hezekiya cewa, “Ga abin da
UBANGIJI, Allah na Isra’ila, ya faɗa. Saboda ka yi addu’a gare ni game da Sennakerib
sarkin Assuriya, 22 ga abin da maganar UBANGIJI ya faɗa a kansa,
“Budurwa Diyar Sihiyona
  ta rena tana kuma maka ba’a.
Diyar Urushalima
  tana kada kai yayinda kake gudu.
23 Wane ne ka zargi ka kuma yi wa saɓo?
  A kan wa ka tā da muryarka
  ka kuma daga idanu cikin fariya?
  A kan Mai Tsarkin nan na Isra’ila!
24 Ta wurin jakadunka
  ka jibge zage-zage a kan Ubangiji.
Ka kuma ce,
  ‘Da kekunan yaƙina masu yawa
na hau ƙwanƙolin duwatsu,
  ƙwanƙolin mafi tsayi na Lebanon.
Na sassare al’ul mafi tsayi
  fir mafi kyau.
Na kai can wuri mafi nisa na kurminsa.
25 Na haƙa rijiyoyi a baƙuwar ƙasa
  na kuma sha ruwa a can.

Da tafin ƙafafuna
na busar da dukan rafuffukan Masar.’

26 “Ba ka ji ba cewa
tun dā can na shirya ya zama haka?
A kwanakin dā na kafa shi;
yanzu na sa ya faru,
cewa ka mai da birane masu mafaka
zuwa tsibin ɓuraguzai.
27 Mutanensu, suka rasa ƙarfi,
sun firgita suka kuma sha kunya.
Suka zama kamar tsire-tsire a gona,
kamar tsire-tsiren ta suka tohu,
kamar ciyawar da ya tsiro a kan rufi,
wadda zafi ya yi wa ƙuna kafin tă yi girma.

28 “Amma na san inda kake zama
da sa’ad da kakan fita ka kuma koma
da yadda ka harzuƙa gāba da ni.
29 Saboda ka harzuƙa gāba da ni
kuma saboda girmankanka ya kai kunnuwana,
zan sa ƙugiya a hancinka
linzamina a bakinka,
zan kuma sa ka koma
ta hanyar da ka zo.
30 “Wannan zai zama alama gare ka, ya Hezekiya,
“Wannan shekara za ka ci abin da ya yi girma da kansa,
shekara ta biyu kuma abin da ya tsiro daga wancan.
Amma a shekara ta uku za ka yi shuki ka kuma girba,
za ka dasa gonakin inabi ka kuma ci ’ya’yansu.
31 Sauran da suka rage na gidan Yahuda kuwa
za su yi saiwa a ƙarƙashi su kuma ba da ’ya’ya a bisa.
32 Gama daga Urushalima raguwa za tă fito,
kuma daga Dutsen Sihiyona ƙungiyar waɗanda suka tsira.
Himmar UBANGIJI Maɗaukaki
zai cika wannan.
33 “Saboda haka ga abin da UBANGIJI yana cewa game da sarkin Assuriya,
“Ba zai shiga wannan birni ba
ya harbe kibiya a nan.
Ba zai zo gabansa da garkuwa ba
ko ya gina mahaurai kewaye a kansa ba.
34 Ta hanyar da ya zo da ita zai koma;
ba zai shiga wannan birni ba,”
in ji UBANGIJI.
35 “Zan kāre wannan birni in kuma cece shi,
saboda girmana da kuma saboda sunan Dawuda bawana!”

*(2 Sarakuna 19.35-37)*

36 Sai mala’ikan UBANGIJI ya fita ya kuma karkashe mutane dubu ɗari da dubu
tamanin da dubu biyar a sansanin Assuriya. Sa’ad da mutane suka farka kashegari,
sai ga gawawwaki duk a kwance! 37 Saboda haka Sennakerib sarkin Assuriya ya
janye. Ya koma zuwa Ninebe ya zauna a can.

38 Wata rana, yayinda yake yin sujada a haikalin allahnsa Nisrok, ’ya’yansa maza
Adrammelek da Sharezer suka kashe shi da takobi, suka kuma gudu zuwa ƙasar
Ararat. Esar-Haddon ɗansa kuwa ya gāje shi a matsayin sarki.

# 38

*Ciwon Hezekiya*
*(2 Sarakuna 20.1-11; 2 Tarihi 32.24-26)*

1 A kwanakin nan sai Hezekiya ya kamu da ciwo ya kuma kusa ya mutu. Annabi
Ishaya ɗan Amoz ya tafi wurinsa ya kuma ce, “Ga abin da Ubangiji ya ce ka shirya
gidanka, domin za ka mutu; ba za ka warke ba.”
2 Hezekiya ya juye fuskarsa wajen bango ya kuma yi addu’a ga Ubangiji, 3 “Ka tuna,
ya Ubangiji, yadda na yi tafiya a gabanka da aminci da dukan zuciya na kuma yi abin
da yake nagari a idanunka.” Sai Hezekiya ya yi kuka mai zafi.
4 Sai maganar Ubangiji ta zo wa Ishaya cewa, 5 “Ka tafi ka faɗa wa Hezekiya,
‘Ga abin da Ubangiji Allah na kakanka Dawuda, ya ce na ji addu’arka na kuma ga
hawayenka; zan ƙara maka shekaru goma sha biyar ga rayuwarka. 6 Zan kuwa cece
ka da wannan birni daga hannun sarkin Assuriya. Zan kiyaye wannan birni.
7 “ ‘Ga alamar Ubangiji gare ka cewa Ubangiji zai aikata kamar yadda ya yi
alkawari. 8 Zan sa inuwar da rana ta yi a kan matakalar Ahaz ta koma baya da
taki goma.’ ” Saboda haka inuwar ta koma da baya daga fuskar rana har taki goma.
9 Rubutun Hezekiya sarkin Yahuda bayan ciwonsa da kuma warkarwarsa.

10 Na ce, “Cikin tsakiyar rayuwata
dole in bi ta ƙofofin mutuwa
a kuma raba ni da sauran shekaruna?”
11 Na ce, “Ba zan ƙara ganin Ubangiji ba,
Ubangiji a ƙasa ta masu rai;
ba zan ƙara ga wani mutum,
ko in kasance tare da waɗanda suke zama a wannan duniya ba.
12 Kamar tentin makiyayi
an rushe gidana aka kuma ƙwace ta daga gare ni.
Kamar mai saƙa, na nannaɗe rayuwata,
ya kuma yanke ni daga sandar saƙa;
dare da rana ka kawo ni ga ƙarshe.
13 Na yi jira da haƙuri har safiya,
amma kamar zaki ya kakkarya ƙasusuwana duka;
dare da rana ka kawo ni ga ƙarshe.
14 Na yi kuka kamar mashirare ko zalɓe,
na yi kuka kamar kurciya mai makoki.
Idanuna suka rasa ƙarfi yayinda na duba sammai.
Na damu; Ya Ubangiji, ka taimake ni!”

15 Amma me zan ce?
Ya riga ya yi mini magana, shi kansa ne kuma ya aikata.
Zan yi tafiya da tawali’u dukan kwanakina
saboda wahalar raina.
16 Ubangiji, ta waɗannan abubuwa ne mutane suke rayuwa;
ruhuna kuma yana samun rai a cikinsu shi ma.
Ka maido mini da lafiya
ka kuma sa na rayu.
17 Tabbatacce wannan kuwa saboda ribata ne
cewa in sha irin wahalan nan.

Cikin ƙaunarka ka kiyaye ni
daga ramin hallaka;
ka sa dukan zunubaina
a bayanka.
18 Gama kabari ba zai yabe ka ba,
matattu ba za su rera yabonka ba;
waɗanda suka gangara zuwa rami
ba za su sa zuciya ga amincinka ba.
19 Masu rai, masu rai, su suke yabonka,
kamar yadda nake yi a yau;
iyaye za su faɗa wa ʼyaʼyansu
game da amincinka.

20 Ubangiji zai cece ni,
za mu kuma rera da kayan kiɗi masu tsirkiya
dukan kwanakinmu
a cikin haikalin Ubangiji.
21 Ishaya ya riga ya ce, "Ku shirya curin da aka yi da ʼyaʼyan ɓaure ku kuma shafa
a marurun, zai kuwa warke."
22 Hezekiya ya riga ya yi tambaya ya ce, "Me zai zama alama ta cewa zan haura
zuwa haikalin Ubangiji?"

# 39

*Jakadu daga Babilon*
*(2 Sarakuna 20.12-19)*

1 A wannan lokaci Merodak-Baladan ɗan Baladan sarkin Babilon ya aika wa
Hezekiya wasiƙu da kuma kyauta, domin ya ji rashin lafiyarsa da kuma warkarwarsa.
2 Hezekiya ya marabci jakadun da murna ya kuma nuna musu abin da gidajen
ajiyarsa sun ƙunsa, azurfa, zinariya, yaji, tatsatsen mai, dukan kayan yaƙinsa da
kuma kome da yake a maʼajinsa. Babu abin da yake a cikin fadansa ko cikin dukan
masarautarsa da Hezekiya bai nuna musu ba.
3 Sai Ishaya annabi ya tafi wurin Sarki Hezekiya ya kuma tambaye shi ya ce, "Mene
ne waɗannan mutane suka faɗa, kuma daga ina suka fito?"
Hezekiya ya amsa ya ce, "Daga ƙasa mai nisa. Sun zo ne daga Babilon."
4 Annabi ya yi tambaya ya ce, "Mene ne suka gani a fadanka?"
Hezekiya ya ce, "Sun ga kome da kome a fadana. Babu abin da ban nuna musu a
cikin maʼajina ba."
5 Sai Ishaya ya ce wa Hezekiya, "Ka ji maganar Ubangiji Maɗaukaki. 6 Tabbatacce
lokaci yana zuwa saʼad da kome da yake cikin fadanka, da kuma dukan abin da
kakanninka suka ajiye har yă zuwa yau, za a kwashe zuwa Babilon babu abin da
za a bari, in ji Ubangiji. 7 Waɗansu cikin zuriyarka, nama da jininka waɗanda za a
haifa maka, za a kwashe su a tafi, za su zama bābānni a fadan sarkin Babilon."
8 Hezekiya ya ce, "Maganar Ubangiji da ka yi tana da kyau." Gama ya yi tunani a
ransa cewa, "Salama da kāriya za su kasance a zamanina."

# 40

*Taʼaziyya don mutanen Allah*

1 Taʼaziyya, ku taʼazantu mutanena,
in ji Allahnku.
2 Yi magana mai kwantar da rai ga Urushalima,

ku kuma furta mata
cewa aiki mai zafinta ya isa,
cewa an fanshi zunubinta,
cewa ta karɓi daga hannun UBANGIJI
ninki biyu saboda dukan zunubanta.

3 Muryar wani tana kira cewa,
“A cikin hamada ku shirya
hanya saboda UBANGIJI;*
ku miƙe manyan hanyoyi domin Allahnmu
a cikin jeji.
4 Za a cike kowane kwari,
a baje kowane dutse da kowane tudu;
za a mayar da karkatattun wurare su zama sumul,
munanan wurare kuma su zama da kyau.
5 Za a kuma bayyana ɗaukakar UBANGIJI,
dukan mutane kuwa za su gan ta.
Gama UBANGIJI da kansa ne ya yi magana.”

6 Muryar tana cewa, “Ka yi shela.”
Na kuwa ce, “Me zan yi shelar?”

“Dukan mutane kamar ciyawa suke,
kuma dukan ɗaukakarsu kamar furannin jeji ne.
7 Ciyawa takan yanƙwane, furanni kuma su yi yaushi,
domin UBANGIJI ya hura iska a kansu.
Tabbatacce mutane ciyawa ne.
8 Hakika ciyawa takan yanƙwane, furanni kuma su yi yaushi,
amma maganar Allahnmu tana nan daram har abada.”

9 Kai da ka kawo labari mai daɗi wa Sihiyona,
ka haura a bisa dutse.
Kai da ka kawo labari mai daɗi wa Urushalima,†
ka tā da muryarka ka yi ihu,
ka ɗaga ta, kada ka ji tsoro;
faɗa wa garuruwan Yahuda,
“Ga Allahnku!”
10 Duba, UBANGIJI Mai Iko Duka yana zuwa da iko,
hannunsa kuma yana yin mulki dominsa.
Duba, ladarsa tana tare da shi,
sakamakonsa kuma na rakiyarsa.
11 Yakan lura da garkensa kamar makiyayi.
Yakan tattara tumaki wuri ɗaya
yă riƙe su kurkusa da ƙirjinsa;
a hankali kuma yakan bi da masu ba da mama.

12 Wane ne ya auna ruwaye a tafin hannunsa,
ko kuwa ya gwada tsawon sammai da fāɗin tafin hannunsa?
Wane ne ya riƙe ƙurar ƙasa a kwando,

* **40:3** Ko kuwa Muryar wani mai kira a cikin hamada. “Ku shirya hanya domin UBANGIJI”. † **40:9** Ko kuwa Ya Sihiyona, mai kawo labari mai daɗi, haura bisa dutse. Ya Urushalima, mai kawo labari mai daɗi

ko kuwa ya auna nauyin duwatsu a magwaji,
tuddai kuma a ma'auni?
13 Wane ne ya fahimci zuciyar‡UBANGIJI,
ko kuwa ya koya masa a matsayin mashawarcinsa?
14 Wane ne UBANGIJI ya nemi shawararsa don yǎ ganar da shi,
wane ne kuma ya koya masa hanyar da ta dace?
Wane ne ya koya masa sani
ko ya nuna masa hanyar fahimta?

15 Tabbatacce al'ummai suna kama da ɗigon ruwa a cikin bokiti
an ɗauke su a matsayin ƙura a kan magwaji;
yakan auna tsibirai sai ka ce ƙura mai laushi.
16 Itatuwan Lebanon ba su isa a yi wutar bagade da su ba,
balle dabbobinsa su isa yin hadayun ƙonawa.
17 A gabansa dukan al'ummai ba kome ba ne;
ya ɗauke su ba a bakin kome ba
kuma banza ne kurum.

18 To, ga wane ne za ka kwatanta Allah?
Wace siffa za ka kwatanta shi da ita?
19 Gunki dai, maƙeri kan yi zubinsa,
maƙerin zinariya kuma yǎ ƙera shi da zinariya
yǎ kuma sarrafa masa sarƙoƙin azurfa.
20 Mutumin da talauci ya sha kansa da ba zai iya miƙa irin hadayar nan ba
kan zaɓi itacen da ba zai ruɓe ba.
Yakan nemi gwanin sassaƙa
don yǎ sassaƙa masa gunkin da ba zai fāɗi ba.

21 Ba ku sani ba?
Ba ku taɓa ji ba?
Ba a faɗa muku daga farko ba?
Ba ku fahimta ba tun kafawar duniya?
22 Yana zaune a kursiyi a bisa iyakar duniya,
kuma mutanenta suna kama da fāra.
Ya miƙa sammai kamar rumfa,
ya kuma shimfiɗa su kamar tentin da za a zauna a ciki.
23 Yakan mai da sarakuna ba kome ba
yǎ mai da masu mulkin wannan duniya wofi.
24 Ba da jimawa ba bayan an shuka su,
ba da jimawa ba bayan an dasa su,
ba da jimawa ba bayan sun yi saiwa a ƙasa,
sai yǎ hura musu iska su yanƙwane,
guguwa kuma ta kwashe su kamar yayi.

25 "Ga wa za ku kwatanta ni?
Ko kuwa wa yake daidai da ni?" In ji Mai Tsarkin nan.
26 Ku ɗaga idanunku ku duba sammai.
Wane ne ya halicce dukan waɗannan?
Wane ne ya fitar da rundunar taurari ɗaya-ɗaya,
yana kiransu, kowanne da sunansa.

‡ **40:13** Ko kuwa Ruhun; Ko kuwa ruhu

Saboda ikonsa mai girma da kuma ƙarfinsa mai girma,
babu ko ɗayansu da ya ɓace.

27 Ya Yaƙub, ya Isra'ila, me ya sa kake ce
kana kuma gunaguni cewa,
"Hanyata tana a ɓoye daga UBANGIJI;
Allah bai kula da abin da yake damuna ba"?
28 Ba ku sani ba?
Ba ku ji ba?
UBANGIJI madawwamin Allah ne,
Mahaliccin iyakokin duniya.
Ba zai taɓa gaji ko yă kasala ba,
kuma fahimtarsa ya wuce gaban ganewar mutum.
29 Yakan ba da ƙarfi ga waɗanda suka gaji
yă kuma ƙara ƙarfi ga marasa ƙarfi.
30 Ko matasa ma kan gaji su kuma kasala,
samari kuma kan yi tuntuɓe su fāɗi;
31 amma waɗanda suka dogara ga UBANGIJI
za su sabunta ƙarfinsu.
Za su yi firiya da fikafikai kamar gaggafa;
za su kuma yi gudu ba kuwa za su gaji ba,
za su yi tafiya ba kuwa za su kasala ba.

# 41

*Mai taimakon Isra'ila*

1 "Ku yi shiru a gabana, ku tsibirai!
Bari al'ummai su sabunta ƙarfinsu!
Bari su zo gaba su yi magana;
bari mu sadu a wurin shari'a.

2 "Wa ya zuga wannan daga gabas,
yana kiransa cikin adalci ga yin hidima?*
Ya miƙa masa al'ummai
ya kuma yi nasara da sarakuna a gabansa.
Ya mai da su ƙura da takobinsa,
zuwa inda iska ke hurawa ta wurin bugun da ya yi musu.
3 Ya fafare su ya kuma yi tafiyarsa lafiya ƙalau,
a hanyar da ƙafafunsa ba su taɓa bi ba.
4 Wane ne ya taɓa yin haka ya kuma sa ya faru,
yana kira ga tsararraki daga farko?
Ni, UBANGIJI ina can tun farkonsu
ni kuma ina can har ƙarshe, Ni ne shi."

5 Tsibirai sun gan shi suka kuma ji tsoro;
iyakokin duniya sun yi rawar jiki.
Suka kusato suka kuma zo gaba;
6 kowa na taimakon wani
yana ce wa ɗan'uwansa, "Ka ƙarfafa!"
7 Masassaƙi yakan ƙarfafa maƙerin zinariya,
kuma shi mai gyara da guduma ya yi sumul

---

* **41:2** Ko kuwa / wanda nasara ke samunsa a kowane mataki

yakan ƙarfafa mai harhaɗawa.
Ya ce game da haɗin, “Ya yi kyau.”
Yakan buga ƙusoshi su riƙe gunkin don kada yă fāɗi.

8 “Amma kai, ya Isra’ila, bawana,
Yaƙub, wanda na zaɓa,
zuriyar Ibrahim abokina,
9 na ɗauke ka daga iyakar duniya,
daga kusurwoyi masu nesa na kira ka.
Na ce, ‘Kai bawana ne’;
na zaɓe ka ban kuwa ƙi ka ba.
10 Saboda haka kada ka ji tsoro, gama ina tare da kai;
kada ka karai, gama ni ne Allahnka.
Zan ƙarfafa ka in kuma taimake ka;
zan riƙe ka da hannun damana mai adalci.

11 “Duk wanda ya yi fushi da kai
tabbatacce zai sha kunya da ƙasƙanci;
waɗanda suka yi hamayya da kai
za su zama kamar ba kome ba su kuma hallaka.
12 Ko ka nemi abokan gābanka,
ba za ka same su ba.
Waɗanda suke yaƙi da kai
za su zama kamar ba kome ba.
13 Gama ni ne Ubangiji Allahnka,
wanda ya riƙe ka da hannun damana
ya kuma ce maka, Kada ka ji tsoro;
zan taimake ka.
14 Kada ka ji tsoro, ya Yaƙub marar ƙarfi,
ya ƙaramin Isra’ila,
gama ni kaina zan taimake ka,” in ji Ubangiji,
Mai Fansarka, Mai Tsarkin nan na Isra’ila.
15 “Duba, zan sa ka cikin abin sussuka,
saboda kuma mai kaifi mai haƙora da yawa.
Za ka yi sussukar duwatsu ka ragargaza su,
ka kuma farfashe tuddai su zama kamar yayi.
16 Za ka tankaɗe su, iska kuma ta kwashe su,
guguwa kuma za tă warwatsa su.
Amma za ka yi farin ciki a cikin Ubangiji
ka kuma ɗaukaka a cikin Mai Tsarkin nan na Isra’ila.

17 “Matalauta da mabukata suna neman ruwa,
amma babu kome;
harsunansu sun bushe saboda ƙishi.
Amma Ni Ubangiji zan amsa musu;
Ni, Allah na Isra’ila, ba zan yashe su ba.
18 Zan sa koguna su malalo a ƙeƙasassun tuddai,
maɓulɓulan ruwa kuma a kwaruruka.
Zan mai da hamada tafkunan ruwa,
busasshiyar ƙasa kuma ta zama maɓulɓulan ruwa.
19 Zan sa a hamada ta tsiro da
al’ul da itacen ƙirya, da itacen ci-zaƙi, da zaitun.
Zan sa itace mai girma a ƙasashe masu sanyi ya tsiro a ƙeƙasasshiyar ƙasa,

tare da fir da kuma saifires,
20 don mutane su gani su kuma sani,
su lura su kuma fahimci,
cewa hannun UBANGIJI ne ya aikata haka,
cewa Mai Tsarkin nan na Isra'ila ya sa abin ya faru.

21 "Ka gabatar da damuwarka," in ji UBANGIJI.
"Ka kawo gardandaminka," in ji Sarki na Yaƙub.
22 "Ka shigar da gumakanka don su faɗa mana
abin da zai faru.
Faɗa mana abubuwan da suka riga suka faru,
domin mu lura da su
mu kuma san abin da zai faru a ƙarshe.
Ko kuwa ku furta mana abubuwan da za su faru,
23 faɗa mana abin da nan gaba ta ƙunsa,
don mu san cewa ku alloli ne.
Ku yi wani abu, mai kyau ko mummuna,
don mu ji tsoro da fargaba.
24 Amma ku ba kome ba ne
kuma ayyukanku banza da wofi ne;
duk wanda ya zaɓe ku abin ƙyama ne.

25 "Na zuga wani daga arewa, ya kuwa zo,
wani daga inda rana ke fitowa wanda yake kira bisa sunana.
Yana takawa a kan masu mulki kamar da taɓarya,
sai ka ce maginin tukwane yana taka laka.
26 Wa ya faɗi wannan tun daga farko, don mu sani,
ko kafin ya faru, don mu ce, 'Ya faɗi daidai'?
Ba wanda ya faɗa wannan,
ba wanda ya riga faɗe shi,
ba wanda ya ji wata magana daga gare ku.
27 Ni ne na farkon da ya ce wa Sihiyona, 'Duba, ga su nan!'
Na ba wa Urushalima saƙon labari mai daɗi.
28 Na duba amma ba kowa
ba wani a cikinsu da zai ba da shawara,
ba wani da zai ba da amsa sa'ad da na tambaye su.
29 Duba, dukansu masu ƙarya ne!
Ayyukansu ba su da riba;
siffofinsu iska ne kawai da ruɗami.

# 42

### *Bawan UBANGIJI*

1 "Ga bawana, wanda na ɗaukaka,
zaɓaɓɓen nan nawa wanda nake jin daɗi;
Zan sa Ruhuna a cikinsa
zai kuwa kawo adalci ga al'ummai.
2 Ba zai yi ihu ko ya tā da murya,
ko ya daga muryarsa a tituna ba.
3 Iwan da ta tanƙware ba zai karye ba,
ba zai kashe lagwani mai hayaƙi ba.
Cikin aminci zai kawo adalci;
4 ba zai kāsa ko ya karai ba

sai ya kafa adalci a duniya.
Cikin dokarsa tsibirai za su sa zuciya.”

5 Ga abin da Allah UBANGIJI ya ce,
shi da ya halicci sammai ya kuma miƙe su,
wanda ya shimfiɗa duniya da dukan abin da ya fito cikinta,
wanda ya ba wa mutanenta numfashi,
da rai ga waɗanda suke tafiya a kanta.
6 “Ni UBANGIJI, na kira ka cikin adalci;
zan riƙe hannunka.
Zan kiyaye ka in kuma sa ka
zama alkawari ga mutane
haske kuma ga Al’ummai,
7 don ka buɗe idanun makafi
ka ’yantar da kamammu daga kurkuku
kuma kunce ɗaurarrun kurkuku masu zama cikin duhu.

8 “Ni ne UBANGIJI; sunana ke nan!
Ba zan ba da ɗaukakata ga wani ba ko yabona ga gumaka.
9 Duba, abubuwan da sun tabbata,
sababbin abubuwa kuwa nake furtawa;
kafin ma su soma faruwa
na sanar da su gare ku.”

### *Waƙar yabo ga UBANGIJI*

10 Ku rera sabuwar waƙa ga UBANGIJI,
ku yi yabonsa daga iyakar duniya,
ku da kuka gangara zuwa teku, da kome da yake cikinsa,
ku tsibirai, da waɗanda suke zama a cikinsu.
11 Bari hamada da garuruwanta su tā da muryoyinsu;
bari wuraren zaman da Kedar ke zama su yi farin ciki.
Bari mutanen Sela su rera don farin ciki;
bari su yi sowa daga ƙwanƙolin duwatsu.
12 Bari su ɗaukaka UBANGIJI
su kuma yi shelar yabonsa a tsibirai.
13 UBANGIJI zai fita ya yi yaƙi kamar mai ƙarfi,
kamar jarumi zai yi himma;
da ihu zai tā da kirarin yaƙi
zai kuma yi nasara a kan abokan gābansa.

14 “Na daɗe ina shiru,
na yi shiru na kuma ƙame kaina.
Amma yanzu, kamar mace mai naƙuda,
na yi ƙara, ina nishi ina kuma haki.
15 Zan lalatar da duwatsu da tuddai
in busar da dukan itatuwansu;
zan mai da koguna su zama tsibirai
in kuma busar da tafkuna.
16 Zan yi wa makafi jagora a hanyoyin da ba su taɓa sani ba,
a hanyoyin da ba a saba ba zan bishe su;
zan mai da duhu ya zama haske a gabansu
in kuma mai da ƙasa mai kururrumai ta zama sumul.
Abubuwan da zan yi ke nan;

ba zan yashe su ba.
17 Amma waɗanda suka dogara ga gumaka,
waɗanda suke ce wa siffofi, 'Ku ne allolinmu,'
za a mai da su baya da kunya.

*Isra'ila makaho da kuma kurma*

18 "Ka ji, kai kurma;
duba, kai makaho, ka kuma gani!
19 Wane ne makaho in ba bawana ba,
da kuma kurma in ba ɗan aikan da na aika ba?
Wane ne makaho kamar wanda ya miƙa kai gare ni,
makaho kamar bawan UBANGIJI?
20 Kun ga abubuwa masu yawa, amma ba ku kula ba;
kunnuwanku suna a buɗe, amma ba kwa jin wani abu."
21 Yakan gamsar da UBANGIJI
saboda adalcinsa
ya sa dokarsa ta zama mai girma da kuma mai ɗaukaka.
22 Amma ga mutanen da aka washe aka kuma kwashe ganima,
an yi wa dukansu tarko a cikin rammuka
ko kuma an ɓoye su cikin kurkuku.
Sun zama ganima,
babu wani da zai kuɓutar da su;
an mai da su ganima,
ba wanda zai ce, "Mayar da su."

23 Wane ne a cikinku zai saurari wannan
ko ya kasa kunne sosai a cikin kwanaki masu zuwa?
24 Wa ya ba da Yaƙub don yă zama ganima
Isra'ila kuma ga masu kwasar ganima?
Ba UBANGIJI ba ne,
wanda kuka yi wa zunubi?
Gama ba su bi hanyoyinsa ba;
ba su yi biyayya da dokarsa ba.
25 Saboda haka ya zuba musu zafin fushinsa,
yaƙi mai tsanani.
Ya rufe su cikin harsunan wuta, duk da haka ba su gane ba;
ya cinye su, amma ba su koyi kome ba.

# 43

*Mai Ceto kaɗai na Isra'ila*

1 To, fa, ga abin da UBANGIJI yana cewa,
shi da ya halicce ka, ya Yaƙub,
shi da ya siffanta ka, ya Isra'ila,
"Kada ka ji tsoro, gama na fanshe ka;
na kira ka da suna; kai nawa ne.
2 Sa'ad da kuka bi ta ruwaye,
zan kasance tare da ku;
sa'ad da kuka bi ta koguna,
ba za su kwashe ku ba.
Sa'ad da kuke tafiyata cikin wuta,
ba za tă ƙone ku ba;
harsunan wutar ba za su ƙone ku ba.

3 Gama ni ne UBANGIJI, Allahnku,
Mai Tsarkin nan na Isra'ila, Mai Cetonku;
na bayar da Masar don fansa,
Kush da Seba a maimakonku.
4 Da yake ku masu daraja da kuma girma ne a idona,
saboda kuma ina ƙaunarku,
zan ba da mutane a maimakonku,
al'umma kuma domin ranku.
5 Kada ku ji tsoro, gama ina tare da ku;
zan kawo yaranku daga gabas
in kuma tattara ku daga yamma.
6 Zan ce wa arewa, 'Ku miƙa su!'
Ga kudu kuma, 'Kada ku riƙe su.'
Kawo 'ya'yana maza daga nesa
'ya'yana mata kuma daga iyakar duniya,
7 kowa da ake kira da sunana,
wanda aka halitta saboda ɗaukakata,
wanda na siffanta na kuma yi."
8 Jagoranci waɗanda suke da idanu amma suke makafi,
waɗanda suke da kunnuwa amma suke kurame.
9 Dukan al'ummai su taru
mutane kuma su tattaru.
Wane ne a cikinsu ya yi faɗar wannan
ya kuma yi mana shelar abubuwan da suka riga suka faru?
Bari su kawo shaidunsu don su tabbatar cewa sun yi daidai,
don waɗansu su ji su kuma ce, "Gaskiya ne."
10 "Ku ne shaiduna," in ji UBANGIJI,
"bawana kuma wanda na zaɓa,
saboda ka sani ka kuma gaskata ni
ka kuma fahimci cewa ni ne shi.
Kafin ni babu allahn da aka siffanta,
ba kuwa za a yi wani a bayana ba.
11 Ni kaɗai, ni ne UBANGIJI,
kuma in ban da ni babu wani mai ceto.
12 Na bayyana na ceci na kuma furta,
Ni ne, ba wani baƙon allah a cikinku.
Ku ne shaiduna," in ji UBANGIJI, "cewa ni ne Allah.
13 I, kuma tun fil azal ni ne shi.
Babu wani da zai amshi daga hannuna.
Sa'ad da na aikata, wa zai iya sauyawa?"

### *Jinƙan Allah da rashin amincin Isra'ila*

14 Ga abin da UBANGIJI yana cewa,
Mai Fansarku, Mai Tsarkin nan na Isra'ila,
"Saboda ku zan aika Babilon
in kawo dukan Babiloniyawa kamar masu gudun hijira,*
a cikin jiragen ruwa waɗanda suke taƙama da su.
15 Ni ne UBANGIJI, Mai Tsarkin nan,
Mahaliccin Isra'ila, Sarkinku."

16 Ga abin da UBANGIJI yana cewa,
shi da ya yi hanya ta cikin teku,

* **43:14** Ko kuwa Kaldiyawa

hanya ta cikin manyan ruwaye,
17 wanda ya ja kekunan yaƙi da dawakai,
mayaƙa da kuma ƙarin mayaƙa tare
ya kwantar da su a can, ba kuwa za su ƙara tashi ba,
ya kashe hayaƙi daga lagwani,
18 “Ku manta da abubuwan da suka riga suka faru;
kada ku yi tunanin abin da ya riga ya wuce.
19 Duba, ina yi abu sabo!
Yanzu yana faruwa; ba ku gan shi ba?
Ina yin hanya a cikin hamada
rafuffuka kuma a cikin ƙeƙasasshiyar ƙasa.
20 Namun jeji suna girmama ni,
diloli da mujiyoyi ma haka,
domin na tanada musu ruwa a hamada
da rafuffuka a ƙeƙasasshiyar ƙasa,
don a ba da abin sha ga mutanena, zaɓaɓɓuna,
21 mutanen da na yi saboda kaina
don su furta yabona.

22 “Duk da haka ba ku kira bisa sunana ba, ya Yaƙub,
ba ku gajiyar da kanku saboda ni ba, ya Isra’ila.
23 Ba ku kawo mini tumaki don hadaya ta ƙonewa ba,
balle ku girmama ni da hadayunku.
Ban nawaita muku da hadaya ta gari ba
balle in gajiyar da ku da bukatar turare.
24 Ba ku saya wani turaren kalamus domina ba
ko ku gamshe ni da kitsen hadayunku.
Amma kun nawaita ni da zunubanku
kuka kuma gajiyar da ni da laifofinku.

25 “Ni kaɗai ne na shafe
laifofinku, saboda sunana,
ban kuma ƙara tunawa da zunubanku ba.
26 Ku tunashe ni abin da ya riga ya wuce,
bari mu yi muhawwara wannan batu tare;
ku kawo hujjarku na nuna rashin laifinku.
27 Mahaifinku na farko ya yi zunubi;
masu magana a madadinku suka yi mini tayarwa.
28 Saboda haka zan kunyata manyan baƙi na haikalinku,
zan tura Yaƙub ga hallaka
Isra’ila kuwa yă zama abin dariya.

# 44

*Isra’ila zaɓaɓɓe*

1 “Amma yanzu ka saurara, ya Yaƙub, bawana,
Isra’ila, wanda zaɓa.
2 Ga abin da UBANGIJI yana cewa,
shi wanda ya yi ka, wanda ya siffanta ka a cikin mahaifa,
wanda kuma zai taimake ka.
Kada ka ji tsoro, ya Yaƙub, bawana,
Yeshurun, wanda na zaɓa.

3 Gama zan zuba ruwa a ƙeƙasasshiyar ƙasa,
rafuffuka kuma a busasshiyar ƙasa;
zan ba da Ruhuna ga ’ya’yanka,
albarkata kuma ga zuriyarka.
4 Za su tsiro kamar ciyawa a wuriyar ruwa,
kamar kurmi kusa da rafuffuka masu gudu.
5 Wani zai ce, ‘Ni na UBANGIJI ne’;
wani kuma zai kira kansa da sunan Yaƙub;
har yanzu wani zai rubuta a hannunsa, ‘Na UBANGIJI,’
ya kuma ɗauki sunan Isra’ila.

### *UBANGIJI, ba gumaka ba*

6 “Ga abin da UBANGIJI yana cewa,
Sarki da kuma Mai Fansar Isra’ila, UBANGIJI Maɗaukaki.
Ni ne farko ni ne kuma ƙarshe;
in ban da ni babu wani Allah.
7 Wane ne kuwa kama da ni? Ya faɗa a ji.
Bari yă yi shela ya kuma nuna shi a gabana
mene ne ya faru tun da na kafa mutanena na dā,
mene ne kuma bai riga ya faru ba,
I, bari yă faɗa abin da zai zo.
8 Kada ku firgita kada kuma ku ji tsoro.
Ban furta wannan na kuma yi faɗar haka tuntuni ba?
Ku ne shaiduna. Akwai wani Allah in ban da ni?
A’a, babu wani Dutse; ban san da wani ba.”

9 Duk masu yin gumaka ba kome ba ne,
da kuma abubuwan da suke ɗauka da daraja banza ne.
Waɗanda za su yi magana a madadinsu makafi ne;
jahilai ne, marasa kunya.
10 Waɗanda suke siffanta allah su kuma yi zubin gunki,
waɗanda ba za su yi musu ribar kome ba?
11 Shi da irinsa za su sha kunya;
masu sassaƙa ba kome ba mutane ne kurum.
Bari su tattaru su ɗauki matsayinsu;
za su firgita su kuma sha mummunan kunya.

12 Maƙeri yakan ɗauki kayan aiki
ya yi aiki da shi a cikin garwashi;
ya ƙera gunki da guduma,
ya gyara shi da hannuwansa masu ƙarfi.
Yakan ji yunwa ya kuma rasa ƙarfi;
yakan sha ruwa ya kuma ji gajiya.
13 Kafinta yakan gwada katako
yă kuma zāna siffar da alli;
yă goge shi da kayan aiki
yă kuma zāna shi da alƙalami.
Yă siffanta shi a kamannin mutum,
mutum cikin dukan darajarsa,
don yă ajiye shi a cikin masujada.
14 Yakan ka da itacen saifires, ko kuwa ya ɗauki saifires ko oak.
Yă bar shi yă yi girma a cikin itatuwan kurmi,

ko yă shuka itacen fir, ruwan sama kuma yă sa yă yi girma.
15 Abin hura wutar mutum ne;
yakan ɗebi waɗansu yă hura wuta don yă ji ɗumi,
ya hura wuta yă gasa burodi.
Amma yakan ƙera zinariya yă kuma yi masa sujada;
yakan yi gunki sa'an nan yă rusuna masa.
16 Rabin katakon yakan ƙone a wuta;
a kansa yakan dafa abincinsa,
yă gasa namansa yă kuma ci sai ya ƙoshi.
Yakan ji ɗumi yă kuma ce,
"Aha! Na ji ɗumi; na gan wutar."
17 Da sauran itacen yakan yi allah, gunkinsa;
yă rusuna masa yă kuma yi sujada.
Yakan yi masa addu'a yă ce,
"Ka cece ni; kai ne allahna."
18 Ba su san kome ba, ba su fahimci kome ba;
an rufe idanunsu don kada su gani,
tunaninsu kuma a rufe don kada su fahimta.
19 Ba wanda yakan dakata ya yi tunani,
ba wanda yake da sani ko fahimi ya ce,
"Da rabinsa na yi amfani da shi don hura wuta;
na ma gasa burodi a kan garwashinsa,
na gasa nama na kuma ci.
Ya kamata in yi abin ƙyama daga abin da ya rage?
Ya kamata in rusuna wa guntun katako?"
20 Yana cin toka, zuciyar da ta ruɗe tana ɓad da shi;
ba zai iya cece kansa ba, ko ya ce,
"Wannan abin da yake hannun dama na ba ƙarya ba ne?"

21 "Tuna da waɗannan abubuwa, ya Yaƙub,
gama kai bawana ne, ya Isra'ila.
Na yi ka, kai bawana ne;
Ya Isra'ila, ba zan manta da kai ba.
22 Na shafe laifofinka kamar girgije,
zunubanka kamar hazon safe.
Ka komo wurina,
gama na kuɓutar da kai."

23 Ku rera don farin ciki, ya sammai, gama UBANGIJI ya aikata wannan;
ku yi sowa, ya duniya a ƙarƙashi.
Ku ɓarke da waƙoƙi, ku duwatsu,
ku jeji da dukan itatuwanku,
gama UBANGIJI ya kuɓutar da Yaƙub,
ya nuna ɗaukakarsa a cikin Isra'ila.

### *Za a zauna a Urushalima*

24 "Ga abin da UBANGIJI yana cewa,
Mai Fansarka, wanda ya yi ka a cikin mahaifa.

"Ni ne UBANGIJI,
wanda ya yi dukan abubuwa,
wanda ya shimfiɗa sammai

ya kuma kafa harsashen duniya da kansa,
25 wanda ya sassāke alamun annabawan ƙarya
ya masu duba suka zama wawaye,
wanda ya tumɓuke koyon masu hikima
ya mai da shi banza,
26 wanda ya tabbatar da maganganun bayinsa
ya kuma cika annabce-annabcen 'yan aikansa,

"wanda ya ce game da Urushalima, 'Za a zauna a cikinta,'
game da garuruwan Yahuda, 'Za a gina su,'
27 wanda ya ce wa zurfin ruwaye, 'Ku bushe,
zan kuma busar da rafuffukanku,'
28 wanda ya yi zancen Sairus ya ce, 'Shi ne makiyayina
zan kuma cika dukan abin da na gan dama;
zai yi zancen Urushalima cewa, "Bari a sāke gina ta,"
game da haikali kuma cewa, "Bari a kafa harsashinsa." '

# 45

1 "Ga abin da UBANGIJI ya faɗa wa shafaffensa,
ga Sairus, wanda hannun damansa yana riƙe da shi
don yă ci al'ummai a gabansa
ya kuma tuɓe makaman sarakuna,
don yă buɗe ƙofofi a gabansa
don kada a kulle ƙofofi.
2 Zan sha gabanka
in baje duwatsu;
zan farfashe ƙofofin tagulla
in kuma kakkarye ƙyamaren ƙarfe.
3 Zan ba ka dukiyar duhu,
arzikin da aka ajiye a asirtattun wurare,
saboda ka san cewa ni ne UBANGIJI,
Allah na Isra'ila, wanda ya kira ka da suna.
4 Saboda sunan Yaƙub bawana,
Isra'ila zaɓaɓɓena,
na kira ka da suna
na ba ka matsayin bangirma,
ko da yake ba ka san ni ba.
5 Ni ne UBANGIJI, kuma babu wani;
in ban da ni babu wani Allah.
Zan ƙarfafa ka,
ko da yake ba ka san ni ba,
6 saboda daga fitowar rana
har zuwa fāɗuwarta
mutane za su san cewa babu wani in ban da ni.
Ni ne UBANGIJI, kuma babu wani.
7 Ni ne na siffanta haske na kuma halicci duhu,
ni ne nake ba da nasara in kuma jawo bala'i;
ni, UBANGIJI ne ke aikata dukan waɗannan abubuwa.

8 "Ku sammai, ku sauko da adalci kamar ruwan sama;

bari gizagizai su zubar da yayyafi kamar adalci.
Bari ƙasa ta buɗe,
bari ceto ya tsiro,
bari adalci ya yi girma tare da shi;
ni, UBANGIJIne, na sa ya faru.

9 “Kaitonka mai gardama da Wanda ya yi ka,
da wanda yake kasko a cikin kasko a ƙasa.
Yumɓu ya iya ce wa magini,
‘Me kake yi?’
Aikinka na iya cewa,
‘Ba shi da hannuwa’?
10 Kaiton wanda yake cewa mahaifinsa,
‘Me ka manta?’
Ko kuwa ga mahaifiyarsa,
‘Me kin haifa?’

11 “Ga abin da UBANGIJI yana cewa,
Mai Tsarkin nan na Isra’ila, da kuma Mahaliccinsa.
Game da abubuwan da ke zuwa,
kun tambaye ni game da ’ya’yana,
ko kuwa kun ba ni umarni game da aikin hannuwana?
12 Ai, ni ne wanda ya yi duniya
na kuma halicci mutum a kanta.
Hannuwana ne sun miƙe sammai;
na umarci rundunar sararin sama.
13 Zan tā da Sairus* cikin adalcina.
Zan sa dukan hanyoyinsa su miƙe.
Zai sāke gina birnina
ya kuma ’yantar da mutanena masu bautar talala,
amma ba don wata haya ko lada ba,
in ji UBANGIJI Maɗaukaki.”
14 Ga abin da UBANGIJI yana cewa,
“Kayayyakin Masar da hajar Kush,†
da waɗannan dogayen Sabenawa,
za su ƙetaro zuwa wurinku
za su kuma zama naku;
za su bi bayanku,
suna zuwa cikin sarƙoƙi.
Za su rusuna a gabanku
su roƙe ku, suna cewa,
‘Tabbas Allah yana tare da ku, babu kuma wani;
babu wani allah.’ ”

15 Tabbatacce kai ne Allah wanda ya ɓoye kanka,
Ya Allah da Mai Ceton Isra’ila.
16 Dukan masu yin gumaka za su sha kunya;
za su fita da kunya gaba ɗaya.
17 Amma UBANGIJI zai ceci Isra’ila
da madawwamin ceto;
ba za ku sāke shan kunya ko ƙasƙanci ba,

* **45:13** Da Ibraniyanci shi † **45:14** Wato, yankin Nilu na Bisa

har abada.

18 Gama ga abin da UBANGIJI yana cewa,
shi da ya halicci sammai,
shi ne Allah;
shi da ya sarrafa ya kuma yi duniya,
ya kafa ta;
bai halicce ta don ta zama ba kome ba,
amma ya yi ta don a zauna a ciki,
ya ce,
"Ni ne UBANGIJI,
kuma babu wani.
19 Ban yi magana asirce ba,
daga wani wuri a ƙasar duhu ba;
ban faɗa wa zuriyar Yaƙub,
'Ku neme ni a banza ba.'
Ni, UBANGIJI maganar gaskiya nake yi;
na furta abin da yake daidai.

20 "Ku tattaru ku zo;
ku taru, ku masu gudun hijira daga al'ummai.
Masu jahilci ne waɗanda suke ɗaukan gumakan katakai suna yawo,
waɗanda suke addu'a ga allolin da ba za su cece su ba.
21 Furta abin da zai kasance, ku gabatar da shi,
bari su yi shawara tare.
Wa ya faɗa wannan tuntuni,
wa ya yi shelar sa a kwanakin dā?
Ba ni ba ne, UBANGIJI?
Kuma babu Allah in ban da ni,
Allah mai adalci da kuma Mai Ceto;
babu wani sai ni.

22 "Ku juyo gare ni ku sami ceto,
dukanku iyakokin duniya;
gama ni ne Allah,
kuma babu wani.
23 Da kaina na rantse,
bakina ya furta cikin dukan mutunci
kalmar da ba za a janye ba.
A gabana kowace gwiwa za tă durƙusa;
ta wurina kowane harshe zai rantse.
24 Za su yi zance game da ni su ce, 'A cikin UBANGIJI kaɗai
akwai adalci da kuma ƙarfafawa.' "
Duk wanda ya yi fushi da shi
zai zo wurinsa ya kuma sha kunya.
25 Amma a cikin UBANGIJI dukan zuriyar Isra'ila
za su sami adalci za su kuwa yi yabo.

# 46

*Allolin Babilon*

1 Bel ya rusuna, Nebo ya durƙusa ƙasa;

ana ɗaukan gumakansu a kan dabbobi ne.*
Siffofin da ake yawo da su nawaya ne,
kayan nauyi masu gajiyarwa.
2 Sun durƙusa suka kuma rusuna tare;
ba su iya kuɓutar da nauyin kaya
su kansu sukan tafi bauta.
3 “Ku kasa kunne gare ni, ya ku gidan Yaƙub,
dukanku waɗanda kuka rage na gidan Isra'ila,
ku da na lura da ku tun da aka yi cikinku,
na kuma riƙe ku tun haihuwarku.
4 Har lokacin da kuka tsufa kuka yi furfura
ni ne shi, ni ne shi wanda zai lura da ku.
Na yi ku zan kuma riƙe ku;
zan lura da ku
in kuma kuɓutar da ku.

5 “Da wa za ku kwatanta ni ko ku ɗauka daidai da ni?
Da wa nake kama da har da za ku kwatanta ni?
6 Waɗansu sukan zubar da zinariya daga jaka
su kuma auna azurfa a ma'auni;
sukan yi haya maƙerin zinariya don yă ƙera allah,
su kuma rusuna su yi masa sujada.
7 Sukan daga shi a kafaɗunsu su kuma ɗauke shi;
sukan kafa shi a tsaye a wurinsa, a can kuwa zai tsaya.
Daga wannan wuri ba zai iya gusawa ba.
Ko da wani ya nemi taimakonsa, ba ya amsawa;
ba zai iya cetonsa daga wahala ba.

8 “Ku tuna da wannan, ku sa shi a zuciya,
ku riƙe shi a zuciya, ku 'yan tawaye.
9 Ku tuna da abubuwan da suka riga suka faru, waɗannan na tun dā;
ni ne Allah, kuma babu wani;
ni ne Allah kuma babu wani kamar ni.
10 Nakan sanar da ƙarshe tun daga farko,
daga fil azal, abin da yake zuwa nan gaba.
Na ce nufina zai tabbata,
kuma zan aikata dukan abin da na gan dama.
11 Daga gabas na kira tsuntsun da yake farauta;
daga can ƙasa mai nesa, wani mutumin da zai cika nufina.
Abin da na riga na faɗa, shi zan sa ya faru;
abin da na shirya, shi zan aikata.
12 Ku kasa kunne, ku masu taurinkai,
ku da kuke nesa da adalci.
13 Ina kawo adalcina kusa,
ba shi da nisa;
kuma cetona ba zai jinkirta ba.
Zan yi wa Sihiyona ceto, darajata ga Isra'ila.

# 47

*Fāɗuwar Babilon*
1 “Ki gangara, ki zauna a ƙura,

* **46:1** Ko kuwa su dabbobi ne da shanu kurum

Budurwa Diyar Babilon;
ki zauna a ƙasa ba tare da rawani ba,
Diyar Babiloniyawa.*
Ba za a ƙara kira ke marar ƙarfi ’yar gata ba.
2 Ɗauki dutsen niƙa ki niƙa gari;
ki kware lulluɓinki.
Ki ɗaga fatarinki ki bar ƙafafunki tsirara,
ki kuma yi ta ratsa cikin rafuffuka.
3 Tsirararki zai bayyana
za a kuma buɗe kunyarki.
Zan ɗauki fansa;
ba zan bar wani ba.”
4 Mai Fansarmu, UBANGIJI Maɗaukaki shi ne sunansa,
shi ne Mai Tsarkin nan na Isra’ila.

5 “Zauna shiru, tafi cikin duhu,
Diyar Babiloniya;
ba za a ƙara kira ke
sarauniyar masarautai.
6 Na yi fushi da mutanena
na ƙazantar da gādona;
na ba su ga hannunki,
ba ki kuwa nuna musu jinƙai ba.
Har ma da tsofaffi
kin jibga musu kaya masu nauyi sosai.
7 Kika ce, ‘Zan ci gaba har abada,
madawwamiyar sarauniya!’
Amma ba ki lura da waɗannan abubuwa
ko ki yi la’akari a kan abin da zai faru ba.

8 “To, yanzu fa, ki kasa kunne, ke mai ƙaunar nishaɗi,
mai zama da rai kwance
kina kuma ce wa kanki,
‘Ni ce, kuma babu wani in ban da ni.
Ba zan taɓa zama gwauruwa
ko in sha wahalar rashin ’ya’ya ba.’
9 Duk waɗannan za su sha kanki
cikin farat ɗaya, a rana guda,
rashin ’ya’ya da gwauranci.
Za su zo a kanki da cikakken minzani,
duk da yawan masu dubanki
da kuma dukan sihirinki.
10 Kin dogara a muguntarki
kika kuma ce, ‘Babu wanda ya gan ni.’
Hikimarki da saninki sun ɓad da ke
sa’ad da kika ce wa kanki, ‘Ni ce, kuma babu wani in ban da ni.’
11 Bala’i zai fāɗo a kanki,
kuma ba za ki san yadda za ki rinjaye shi yă janye ba.
Masifa za tă fāɗo a kanki
da ba za ki iya tsai da ita da kuɗin fansa ba;
lalacewar da ba ki taɓa mafarkinta ba
za tă auko miki nan da nan.

* **47:1** Ko kuwa Kaldiyawa; haka ma a aya 5.

12 “Ki dai ci gaba, da sihirinki
da kuma makarunki masu yawa,
waɗanda kika yi ta wahala tun kina jaririya.
Mai yiwuwa ki yi nasara,
mai yiwuwa ki jawo fargaba.
13 Dukan shawarwarin da kika samu sun dai gajiyar da ke ne kawai!
Bari masananki na taurari su zo gaba,
waɗannan masu zāna taswirar sammai suna kuma faɗa miki dukan abin da zai faru da ke wata-wata,
bari su cece ki daga abin da zai faru da ke.
14 Tabbas suna kama da bunnu;
wuta za tă cinye su ƙaf.
Ba za su ma iya ceton kansu
daga ikon wutar ba.
Ba wutar da wani zai ji ɗumi;
ba wutar da za a zauna kusa da ita.
15 Abin da za su iya yi miki ke nan kawai,
waɗannan da kika yi ta fama da su
kika kuma yi ciniki da su tun kina jaririya.
Kowannensu zai tafi cikin kuskurensa;
babu ko ɗayan da zai cece ki.

# 48

*Isra’ila mai taurinkai*

1 “Ku kasa kunne ga wannan, ya gidan Yaƙub,
waɗanda ake kira da sunan Isra’ila
suka kuma fito daga zuriyar Yahuda,
ku da kuke yin rantsuwa da sunan UBANGIJI
kuna kuma kira sunan Allah na Isra’ila,
amma ba da gaskiya ko adalci ba,
2 ku da kuke kiran kanku ’yan ƙasar birni mai tsarki
kuna kuma dogara ga Allah na Isra’ila,
UBANGIJI Maɗaukaki ne sunansa,
3 na nanata abubuwan da suka riga suka faru tuntuni,
bakina ya yi shelar su na kuma sanar da su;
sai nan da nan na aikata, suka kuma faru.
4 Gama na san yadda kuke da taurinkai;
jijiyoyin wuyanku ƙarafa ne,
goshinku tagulla ne.
5 Saboda haka na faɗa waɗannan abubuwa tuntuni;
kafin su faru na yi shelarsu gare ku
saboda kada ku ce,
‘Gumakana ne suka yi su;
siffar itacena da allahn zinariyana ne ya ƙaddara su.’
6 Kun riga kun ji waɗannan abubuwa; kuka gan su duka.
Ba za ku yarda da su ba?

“Daga yanzu zuwa gaba zan faɗa muku sababbin abubuwa,
na ɓoyayyun abubuwan da ba ku sani ba.
7 Yanzu an halicce su, ba da daɗewa ba;
ba ku riga kun ji game da su kafin yau ba.

Saboda haka ba za ku ce,
'I, na san da su ba.'
8 Ba ku ji ko balle ku gane ba;
tun da kunnenku bai buɗu ba.
Tabbatacce na san yadda kun zama masu tayarwa;
an kira ku 'yan tawaye daga haihuwa.
9 Saboda girman sunana na jinkirta fushina;
saboda girman yabona na janye shi daga gare ku,
don dai kada a yanke ku.
10 Duba, na tace ku, ko da yake ba kamar azurfa ba;
na gwada ku cikin wutar wahala.
11 Saboda girmana, saboda girmana, na yi haka.
Yaya zan ƙyale a ƙazantar da kaina?
Ba zan raba ɗaukakata da wani ba.

### *An 'yantar da Isra'ila*

12 "Ka kasa kunne gare ni, ya Yaƙub,
Isra'ila, wanda na kira cewa,
Ni ne shi;
ni ne na farko ni ne kuma na ƙarshe.
13 Hannuna ne ya kafa harsashen duniya,
hannuna na dama kuma ya shimfiɗa sammai;
sa'ad da na kira su,
duka suka miƙe tsaye gaba ɗaya.

14 "Ku tattaru, dukanku ku kuma saurara,
Wanne a cikin gumakan ya iya faɗa waɗannan abubuwa?
Zaɓaɓɓen da UBANGIJI yake ƙauna
zai aikata nufinsa a kan Babilon;
hannunsa zai yi gāba da Babiloniyawa.*
15 Ni kaina, na faɗa;
I, na kira shi.
Zan kawo shi,
zai kuma yi nasara a cikin aikinsa.
16 "Ku zo kusa da ni ku kuma saurari wannan.
"Daga farkon shela ban yi magana a ɓoye ba;
a lokacin da ya faru, ina nan a wurin."

Yanzu kuwa UBANGIJI Mai Iko Duka ya aiko ni,
da Ruhunsa.

17 Ga abin da UBANGIJI yana cewa,
Mai Fansarku, Mai Tsarkin nan na Isra'ila ya ce,
"Ni ne UBANGIJI Allahnku,
wanda ya koya muku abin da ya fi muku kyau,
wanda ya muku hanyar da za ku bi.
18 Da a ce kawai za ku mai da hankali ga umarnaina,
da salamarku ta zama kamar kogi,
adalcinku kamar raƙuman teku.
19 Da zuriyarku ta zama kamar yashi,
'ya'yanku kamar tsabar hatsin da ba a iya ƙidayawa;

* **48:14** Ko kuwa Kaldiyawa; haka ma a aya 20.

da ba za a taɓa yanke sunansu
balle a hallaka su daga gabana ba."

20 Ku bar Babilon,
ku gudu daga Babiloniyawa!
Ku yi shelar wannan da sowa ta farin ciki
ku kuma furta shi.
Ku aika shi zuwa iyakokin duniya;
ku ce, "UBANGIJI ya fanshi bawansa Yaƙub."
21 Ba su ji ƙishi ba sa'ad da ya bishe su a cikin hamada;
ya sa ruwa ya malalo dominsu daga dutse;
ya tsage dutse
ruwa kuwa ya kwararo.

22 "Babu salama ga mugaye" in ji UBANGIJI.

# 49

*Bawan UBANGIJI*

1 Ku kasa kunne gare ni, ku tsibirai;
ku ji wannan, ku al'ummai masu nesa.
Kafin a haife Ni UBANGIJI ya kira ni;
tun daga haihuwata ya ambaci sunana.
2 Ya yi bakina kamar takobi mai kaifi,
cikin inuwar hannunsa ya ɓoye ni;
ya sa na zama kamar kibiya mai tsini
ya kuma ɓoye ni cikin kwarinsa.
3 Ya ce mini, "Kai bawana ne,
Isra'ila, a cikinka zan bayyana darajata."
4 Amma na ce, "Na yi aiki a banza;
na kashe duk ƙarfina a banza da wofi.
Duk da haka abin da yake nawa yana a hannun UBANGIJI,
ladana kuma tana a wurin Allahna."
5 Yanzu fa UBANGIJI ya ce
ya siffanta ni a cikin mahaifa don in zama bawansa
don in dawo da Yaƙub gare shi
in kuma tattara Isra'ila gare shi,
gama an girmama ni a gaban UBANGIJI
Allahna kuma ne ƙarfina
6 ya ce,
"Dan ƙaramin abu ne ka zama bawana
don ka maido da kabilar Yaƙub
ka kuma dawo da waɗannan na Isra'ilawan da na kiyaye.
Zan kuma mai da kai haske ga Al'ummai,
don ka kawo cetona zuwa iyakokin duniya."

7 Ga abin da UBANGIJI yana cewa,
Mai Fansa da kuma Mai Tsarkin nan na Isra'ila
gare shi wanda al'ummai suka rena suka kuma ki,
ga bawan masu mulki.
"Sarakuna za su gan ka su kuma miƙe tsaye,
sarakuna za su gani su kuma rusuna,

saboda UBANGIJI, wanda yake mai aminci,
Mai Tsarkin nan na Isra'ila, wanda ya zaɓe ka."

*Maidowar Isra'ila*

8 Ga abin da UBANGIJI yana cewa,
"A lokacin tagomashina zan amsa muku,
kuma a ranar ceto zan taimake ku;
zan kiyaye ku zan kuma sa
ku zama alkawari ga mutane,
don ku maido da ƙasa
ku kuma sāke raba gādon kufai,
9 don ku ce wa waɗanda suke cikin kurkuku, 'Ku fito,'
ga waɗanda suke cikin duhu kuma, 'Ku 'yantu!'

"Za su yi kiwo kusa da hanyoyi
su kuma sami wurin kiwo a kowane tudu.
10 Ba za su taɓa jin yunwa ko ƙishi ba,
ba kuwa zafin hamada ko rana ta buge su ba.
Shi da ya yi musu jinƙai zai jagorance su
ya kuma bishe su kusa da maɓulɓulan ruwa.
11 Zan mayar da dukan duwatsu su zama hanyoyi,
a kuma gyara manyan hanyoyina.
12 Duba, za su zo daga nesa
waɗansu daga arewa, waɗansu daga yamma,
waɗansu daga yankin Aswan."*

13 Ku yi sowa don farin ciki, ya ku sammai;
ki yi farin ciki, ya ke duniya;
ku ɓarke da waƙa, ya ku duwatsu!
Gama UBANGIJI ya ta'azantar da mutanensa
zai kuma ji tausayin mutanensa da suke shan wahala.

14 Amma Sihiyona ta ce, "UBANGIJI ya yashe ni,
Ubangiji ya manta da ni."

15 "Yana yiwuwa mahaifiya ta manta da jariri a ƙirjinta
ta kuma kāsa nuna tausayi ga yaron da ta haifa?
Mai yiwuwa ta manta,
amma ba zan taɓa manta da ke ba!
16 Duba, na zāna ki a tafin hannuwana;
katangarki kullum suna a gabana.
17 'Ya'yanki maza su komo da gaggawa,
waɗanda suka lalatar da ke kuwa za su bar ki.
18 Ki ɗaga idanunki ki duba kewaye;
dukan 'ya'yanki sun taru suka kuma dawo gare ki.
Muddin ina raye," in ji UBANGIJI,
"Za ki yafa su duka kamar kayan ado;
za ki yi ado da su, kamar amarya.

19 "Ko da yake an lalatar da ke aka kuma mai da ke kufai

* **49:12** Littattafan Bahar Rum; Rubuce-rubucen Masoretik suna da Sinim

ƙasarki kuma ta zama kango,
yanzu za ki kāsa sosai saboda yawan mutanenki,
kuma waɗanda suka cinye ki za su kasance can da nisa.
20 ’Ya’yan da aka haifa a lokacin baƙin cikinki
za su ce a kunnenki,
‘Wannan wuri ya yi mana kaɗan ƙwarai;
ki ƙara mana wurin zama.’
21 Sa’an nan za ki ce a zuciyarki,
‘Wa ya haifa waɗannan?
Na yi baƙin ciki na kuma zama wadda ba ta haihuwa;
an yi mini daurin talala aka kuma ƙi ni.
Wane ne ya yi renon waɗannan?
An bar ni ni kaɗai,
amma waɗannan, ina suka fito?’ ”
22 Ga abin da Ubangiji Mai Iko Duka ya ce,
“Duba, zan yi alama wa Al’ummai,
zan ɗaga tutana wa mutane;
za su kawo ’ya’yanki maza a hannuwansu
su riƙe ’ya’yanki mata a kafaɗunsu.
23 Sarakuna za su zama kamar iyayen reno,
sarauniyoyinsu kuma za su yi renonku kamar uwaye.
Za su rusuna a gabanki da fuskokinsu har ƙasa;
za su lashe ƙura a ƙafafunki.
Sa’an nan za ki san cewa ni ne Ubangiji;
waɗanda suke sa zuciya gare ni ba za su sha kunya ba.”
24 Za a iya ƙwace ganima daga jarumawa,
ko a kuɓutar da kamammu daga hannun marasa tsoro?
25 Amma ga abin da Ubangiji yana cewa,
“I, za a ƙwace kamammu daga jarumawa,
a kuma karɓe ganima daga hannun marasa tsoro;
zan gwabza da waɗanda suke gwabzawa da ke,
zan kuwa ceci ’ya’yanki.
26 Zan sa masu zaluntarki su ci naman jikinsu;
za su bugu da jininsu, sai ka ce sun sha ruwan inabi.
Sa’an nan dukan mutane za su sani
cewa ni, Ubangiji, ni ne Mai Cetonki,
Mai Fansarki, Maɗaukakin nan na Yaƙub.”

# 50

*Zunubin Isra’ila da kuma biyayyar bawa*

1 Ga abin da Ubangiji yana cewa,
“Ina takardar shaida na saki mahaifiyarka daga aure
wadda na kora?
Ko kuwa ga wanda mutumin da nake bin bashi ne
na sayar da kai?
Saboda zunubanka aka sayar da kai;
saboda laifofinka ne ya sa aka kori mahaifiyarka.
2 Sa’ad da na zo, me ya sa babu kowa?
Sa’ad da na yi kira, me ya sa babu wani da ya amsa?
Hannuna ya kāsa ne sosai don fansarka?
Na rasa ƙarfin kuɓutar da kai ne?

Ta wurin tsawatawa kawai na busar da teku,
na mai da koguna hamada;
kifayensu duk sun ruɓe saboda rashin ruwa
suka kuma mutu saboda ƙishi.
3 Na suturar da sararin sama da duhu
na kuma mai da tsummoki abin rufuwarsa."

4 UBANGIJI Mai Iko Duka ya ba ni harshen umarni,
don in san maganar da za tă ƙarfafa gajiyayye.
Ya farkar da ni da safe,
ya farkar da kunnena don in saurara kamar wanda ake koya masa.
5 UBANGIJI Mai Iko Duka ya buɗe kunnuwana,
kuma ban yi tayarwa ba;
ban ja da baya ba.
6 Na ba da bayana ga masu dūkana,
kumatuna ga masu jan gemuna;
ban ɓoye fuskata
daga masu ba'a da masu tofa mini miyau ba.
7 Gama UBANGIJI Mai Iko Duka zai taimake ni,
ba zan sha kunya ba.
Saboda haka na kafa fuskata kamar dutsen ƙanƙara,
na kuma sani ba zan sha kunya ba.
8 Gama shi da zai tabbatar da ni, marar laifi ne yana kusa.
Wane ne zai kawo ƙararraki game da ni?
Bari mu je ɗakin shari'a tare!
Wane ne mai zargina?
Bari yă kalubalance ni!
9 UBANGIJI Mai Iko Duka ne zai taimake ni.
Wane ne zai iya tabbatar da ni mai laifi?
Duk za su koɗe kamar riga;
asu za su cinye su.

10 Wane ne a cikinku yake tsoron UBANGIJI
yana kuma yin biyayya ga maganar bawansa?
Bari wanda yake tafiya cikin duhu,
wanda ba shi da haske,
ya dogara a sunan UBANGIJI ya kuma dogara ga Allahnsa.
11 Amma yanzu fa, dukanku waɗanda kuke ƙuna wuta
kuna kuma tanada wa kanku fitilu masu ci,
ku je ku yi tafiya a cikin hasken wutarku
da na fitilun da kuka ƙuna.
Abin da za ku karɓa ke nan daga hannuna.
Za ku kwanta a cikin azaba.

# 51

*Madawwamin ceto domin Sihiyona*

1 "Ku kasa kunne gare ni, ku da kuna neman adalci
kuke kuma neman UBANGIJI.
Dubi dutse daga inda aka yanke ku
da kuma mahaƙar duwatsu inda aka fafe ku;
2 dubi Ibrahim, mahaifinku,
da Saratu, wadda ta haife ku.

Sa’ad da na kira shi kaɗai ne,
na kuma albarkace shi na kuma mai da shi da yawa.
3 Tabbatacce UBANGIJI zai ta’azantar da Sihiyona
zai kuma duba da tausayi a kan dukan kufanta;
zai sa hamadanta ta zama kamar Eden,
ƙeƙasasshiyar ƙasarta kamar lambun UBANGIJI.
Za a sami farin ciki da murna a cikinta,
godiya da ƙarar rerawa.

4 “Ku kasa kunne gare ni, mutanena;
ku ji ni, al’ummata.
Doka za tă fito daga gare ni;
shari’ata za tă zama haske ga al’ummai.
5 Adalcina na zuwa da sauri,
cetona yana a kan hanya,
hannuna kuma zai kawo adalci ga al’ummai.
Tsibirai za su dube ni
su kuma jira da sa zuciya don hannuna.
6 Ku daga idanunku zuwa sammai
ku dubi duniya a ƙasa;
sammai za su ɓace kamar hayaƙi,
duniya za tă shuɗe kamar riga
mazaunanta kuma su mutu kamar ƙudaje.
Amma cetona zai dawwama har abada,
adalcina ba zai taɓa kāsa ba.

7 “Ku ji ni, ku da kuka san abin da yake daidai,
ku mutanen da kuke da dokata a zukatanku.
Kada ku ji tsoron ba’ar da mutane suke yi
ko ku firgita saboda zargin da suke yi.
8 Gama asu za su cinye su kamar riga;
tsutsotsi za su cinye su kamar ulu.
Amma adalcina zai dawwama har abada,
cetona har dukan zamanai.”

9 Ka tashi, ka tashi! Ka yafa wa kanka ƙarfi,
Ya hannun UBANGIJI;
ka farka, kamar a kwanakin da suka wuce,
kamar a zamanai na dā.
Ba kai ba ne wanda ya yayyanka Rahab gunduwa-gunduwa,
wanda ya soki dodon ruwan nan?
10 Ba kai ba ne ka busar da teku,
ka busar da ruwan zurfafa masu girma,
wanda ya yi hanya a cikin zurfafan teku
saboda fansassu su ƙetare?
11 Waɗanda UBANGIJI ya fansar za su dawo.
Za su shiga Sihiyona da waƙoƙi;
madawwamin farin ciki zai rufe kansu da rawani.
Murna da farin ciki zai cika su,
baƙin ciki da nishi zai ɓace.

12 “Ni kaɗai ne na ta’azantar da ku.
Wane ne ku da kuke tsoron mutane masu mutuwa,

'ya'yan mutane waɗanda suke ciyawa ne kawai,
13 har da kuka manta da UBANGIJI Mahaliccinku,
wanda ya shimfiɗa sammai
ya kuma kafa harsashen duniya,
har kuna zama da tsoro kowace rana
saboda fushin masu zalunci,
waɗanda sun ƙudura sai sun hallaka?
Gama ina fushin mai zalunci?
14 Ba da daɗewa za a 'yantar da 'yan kurkuku;
ba za su mutu a kurkuku ba,
ba kuwa za su rasa abinci ba.
15 Gama ni ne UBANGIJI Allahnku,
wanda ya dama teku domin raƙumansa su yi ruri,
UBANGIJI Maɗaukaki ne sunansa.
16 Na sa maganata a bakinka
na kuma rufe ka da inuwar hannuna,
Na shimfiɗa sammai,
na kafa harsashen duniya,
na kuma ce wa Sihiyona, 'Ku mutanena ne.' "

### *Kwaf na fushin UBANGIJI*

17 Ki farka, ki farka!
Ki tashi, ya Urushalima,
ke da kika sha daga hannun UBANGIJI
kwaf na fushinsa,
ke da kika shanye har ƙasar kwaf
kwaf da ya sa mutane suna tangaɗi.
18 Cikin dukan 'ya'yan da ta haifa;
cikin dukan 'ya'yan da ta yi reno
babu wani da zai kama hannunta.
19 Waɗannan masifu riɓi biyu sun auko miki,
wa zai ta'azantar da ke?
Lalaci da hallaka, yunwa da takobi,
wa zai ƙarfafa ki?
20 'Ya'yanki sun sume;
sun kwanta kusurwar kowane titi,
kamar barewar da aka kama da tarko.
Sun cika da fushin UBANGIJI
da kuma tsawatawar Allahnki.

21 Saboda haka ki ji wannan, ke mai wahala,
wadda ta bugu, amma ba da ruwan inabi.
22 Ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa,
Allahnki, wanda ya kāre mutanensa,
"Duba, na ƙwace daga hannunki
kwaf da ya sa ki tangaɗi;
daga wannan kwaf, kwaf na fushina,
ba za ki ƙara sha ba.
23 Zan sa shi a hannuwan masu gwada miki azaba,
waɗanda suke ce miki,
'Fāɗi rubda ciki don mu iya taka a kanki.'
Kika kuma mai da bayanki kamar ƙasa,
kamar titin da ake takawa a kai."

# 52

1 Ki farka, ki farka, ya Sihiyona,
ki sanya wa kanki ƙarfi.
Ki sa rigarki na daraja,
Ya Urushalima, birni mai tsarki.
Marasa kaciya da maƙazanta
ba za su shi cikinki ba.
2 Ki kakkaɓe ƙurarki;
ki tashi, ki zauna a kursiyinki, ya Urushalima.
Ki ʼyantar da kanki daga sarƙoƙi a wuyanki,
Ke kamammiyar Diyar Sihiyona.
3 Gama ga abin UBANGIJI yana cewa,
“An sayar da ke ba da kuɗi ba,
kuma ba da kuɗi za a fanshe ki ba.”
4 Gama ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa,
“Da farko mutanena suka gangara zuwa Masar don su zauna;
a baya-bayan nan, Assuriya sun zalunce su.
5 “Yanzu kuma me nake da shi a nan?”
In ji UBANGIJI.
“Gama an kwashe mutanena ba a bakin kome ba
kuma waɗanda suka mallake su sun yi musu baʼa,
Kullum ana cin gaba da yin wa sunana saɓo.
6 Saboda haka mutanena za su san sunana;
saboda haka a wannan rana za su san
cewa ni ne wanda ya faɗa wannan.
I, ni ne.”

7 Me ya fi wannan kyau a kan duwatsu
a ga ƙafafu na masu kawo labari mai daɗi
waɗanda suke shelar salama,
waɗanda suke kawo labari mai daɗi,
waɗanda suke shelar ceto,
waɗanda suke ce wa Sihiyona,
“Allahnki yana mulki!”
8 Ki kasa kunne! Masu tsaronki sun tā da muryoyinsu;
tare sun yi sowa ta farin ciki.
Saʼad da UBANGIJI ya komo Sihiyona,
za su gan shi da idanunsu.
9 Ku ɓarke cikin waƙoƙin farin ciki gaba ɗaya,
kangonki na Urushalima,
gama UBANGIJI ya taʼazantar da mutanensa,
ya fanshi Urushalima.
10 UBANGIJI zai nuna hannunsa mai tsarki a fili
a idanun dukan alʼummai,
da kuma dukan iyakokin duniya za su gani
ceton Allahnmu.

11 Ku fita, ku fita daga can!
Kada ku taɓa wani abu marar tsarki!
Ku fita daga cikinta ku zama da tsarki,
ku da kuke ɗaukan kayan aikin UBANGIJI.
12 Amma ba za ku fita a gaggauce ba

ko ku tafi da gudu;
gama UBANGIJI zai ja gabanku,
Allah na Isra'ila zai kasance mai tsaron bayanku.

*Wahala da kuma ɗaukakar bawan*

13 Duba, bawana zai aikata abubuwa da hikima;*
za a tā da shi a kuma ɗaga shi da ɗaukaka ƙwarai.
14 Kamar dai yadda aka kasance da mutane masu yawa waɗanda suka giggice sa'ad da suka gan shi,
kamanninsa ya lalace ƙwarai fiye da na kowane mutum
siffarsa kuma ta yi muni fiye da yadda ta mutum take,
15 haka zai ba al'ummai masu yawa mamaki,
sarakuna kuma za su riƙe bakunansu don mamaki.
Gama abin da ba a faɗa musu ba, shi za su gani,
kuma abin da ba su ji ba, shi za su fahimta.

# 53

1 Wa ya gaskata saƙonmu
kuma ga wa hannun UBANGIJI ya bayyana?
2 Ya yi girma kamar dashe marar ƙarfi,
kamar saiwa kuma daga ƙeƙasasshiyar ƙasa.
Ba shi da kyan gani ko wani makamin da zai ja hankalinmu,
babu wani abin da yake da shi da zai sa mu yi sha'awarsa.
3 Mutane suka rena shi suka ƙi shi,
mutum ne cike da baƙin ciki, ya kuma saba da wahala.
Kamar wanda mutane suna ɓuya fuskokinsu daga gare shi
aka rena shi aka yi banza da shi.
4 Tabbatacce ya ɗauki cututtukanmu
ya kuma daure da baƙin cikinmu
duk da haka muka ɗauka Allah ya hukunta shi ne,
ya buge shi ya kuma sa ya sha azaba.
5 Amma aka yi masa rauni saboda laifofinmu,
aka ƙuje shi saboda kurakuranmu;
hukuncin da ya kawo mana salama ya kasance a kansa,
kuma ta wurin mikinsa ya sa muka warke.
6 Dukanmu, muna kama da tumakin da suka ɓata,
kowannenmu ya kama hanyarsa;
UBANGIJI kuwa ya sa hukunci ya auko a kansa
hukuncin da ya wajaba a kanmu.

7 Aka wulaƙanta shi aka kuma yi masa azaba,
duk da haka bai buɗe bakinsa ba;
aka kai shi kamar ɗan rago zuwa wurin yanka,
kuma kamar tunkiya a gaban masu askinta tana shiru,
haka bai buɗe bakinsa ba.
8 Da wulaƙanci* da kuma hukunci aka ɗauke shi aka tafi.
Wa kuwa zai yi maganar zuriyarsa?
Gama an kawar da shi daga ƙasar masu rai;

---

* **52:13** Ko kuwa zai yi nasara * **53:8** Ko kuma Daga kamawa

saboda laifin mutanena aka kashe shi.†
9 Aka yi jana'izarsa tare da mugaye,
aka binne shi tare da masu arziki,
ko da yake bai taɓa yin wani tashin hankali ba,
ko a sami ƙarya a bakinsa.

10 Duk da haka nufin UBANGIJI ne a ƙuje shi yă kuma sa yă sha wahala,
kuma ko da yake UBANGIJI ya sa ransa ya zama hadaya don zunubi,
zai ga zuriyarsa zai kuma kawo masa tsawon rai,
nufin UBANGIJI kuma zai yi nasara a hannunsa.
11 Bayan wahalar ransa,
zai ga hasken rai, ya kuma gamsu;
ta wurin saninsa bawana mai adalci zai 'yantar da mutane masu yawa,
zai kuma ɗauki laifofinsu.
12 Saboda haka zan ba shi rabo tare da manya,
zai kuma raba ganima tare da masu ƙarfi,
domin ya ba da ransa har mutuwa,
aka kuma lissafta shi tare da masu laifofi.
Gama ya ɗauki zunubin mutane masu yawa,
ya kuma yi roƙo saboda laifofinsu.

# 54

*Ɗaukakar nan gaba ta Sihiyona*

1 "Ki rera, ya ke bakararriya,
ke da ba ki taɓa haihuwa ba;
ki ɓarke da waƙa, ki yi sowa don farin ciki,
ke da ba ki taɓa naƙuda ba;
domin 'ya'yan mace mai kaɗaici sun fi na mai miji yawa,"
in ji UBANGIJI.
2 "Ki fadada wurin tentinki,
ki miƙe labulen tentinki da fāɗi,
kada ki janye;
ƙara tsawon igiyoyinta,
ki kuma ƙara ƙarfin turakunta.
3 Gama za ki fadada zuwa dama da hagu;
zuriyarki za su kori al'ummai
su kuma zauna a kufan biranensu.

4 "Kada ki ji tsoro; ba za ki sha kunya ba.
Kada ki ji tsoron wulaƙanci, ba za a ƙasƙantar da ke ba.
Za ki manta da kunyar ƙuruciyarki
ba kuwa za ki tuna da zargin zaman gwauruwarki ba.
5 Gama Mahaliccinki shi ne mijinki,
UBANGIJI Maɗaukaki ne sunansa,
Mai Tsarkin nan na Isra'ila ne Mai Fansarki;
ana ce da shi Allahn dukan duniya.
6 UBANGIJI zai kira
sai ka ce ke mace ce da aka yashe ta tana kuma damuwa a ranta,
macen da ta yi aure a ƙuruciya,

† **53:8** Ko kuwa kawar. Duk da haka wane ne a zamaninsa ya kula cewa an yanke shi daga ƙasar masu rai saboda laifin mutanena, waɗanda ya kamata su sha bugun?

sai kawai aka ƙi ta," in ji Allahnki.
7 "Gama a ɗan ƙanƙanen lokaci na rabu da ke,
amma da ƙauna mai zurfi zan sāke dawo da ke.
8 Cikin fushi mai zafi
na ɓoye fuskata daga gare ki na ɗan lokaci,
amma da madawwamin alheri
zan ji tausayinki,"
in ji UBANGIJI Mai Fansarki.

9 "A gare ni wannan ya yi kamar kwanakin Nuhu,
sa'ad da na rantse cewa ruwan Nuhu ba za su ƙara rufe duniya ba.
Yanzu fa na rantse ba zan yi fushi da ke ba,
ba zan ƙara tsawata miki kuma ba.
10 Ko da duwatsu za su girgiza
a kuma tumɓuke tuddai,
duk da haka madawwamiyar ƙaunata da nake yi miki ba za tă jijjigu ba
ba kuwa za a kawar da alkawarin salamata ba,"
in ji UBANGIJI, wanda ya ji tausayinki.

11 "Ya ke birni mai shan azaba, wadda hadari ya bulale ki ba a kuma ta'azantar da ke ba,
zan gina ke da duwatsu turkuwoyis,*
zan kafa harsashenki da duwatsun saffaya.†
12 Zan gina hasumiyarki da jan yakutu,
ƙofofinki kuma da duwatsu masu haske,
dukan katangarki kuma da duwatsu masu daraja.
13 UBANGIJI zai koya wa dukan 'ya'yanki maza,
da girma kuma salamar 'ya'yanki zai zama.
14 Da adalci za a kafa ke.
Zalunci zai yi nesa da ke;
ba za ki kasance da wani abin da za ki ji tsoro ba.
Za a kawar da duk wani abin banrazana;
ba zai yi kusa da ke ba.
15 In wani ya far miki, ba daga wurina ba ne;
duk wanda ya far miki zai miƙa wuya gare ki.

16 "Duba, ni ne wanda na halicci maƙeri
wanda yake zuga garwashi ya zama harshen wuta
ya kuma ƙera makamin da ya dace da aikinsa.
Ni ne kuma na halicci mai hallakarwa ya yi ɓarna;
17 ba makamin da aka ƙera don yă cuce ki da zai yi nasara,
za ki kuma mayar da magana ga duk wanda ya zarge ki.
Wannan ne gādon bayin UBANGIJI,
kuma wannan ita ce nasararsu daga gare ni,"
in ji UBANGIJI.

# 55

*Gayyata ga masu jin ƙishi*

1 "Ku zo, dukanku masu jin ƙishi,
ku zo wurin ruwaye;

* **54:11** Ma'anar kalmar Ibraniyancin nan ba ta da tabbas. † **54:11** Ko kuwa lafis lazuli

ku kuma da ba ku da kuɗi,
ku zo, ku saya ku kuma ci!
Ku zo, ku saya ruwan inabi da madara
ba tare da kuɗi ba ba za ku kuma biya kome ba.
2 Don me za ku kashe kuɗi a kan abin da ba abinci ba,
ku kuma yi wahala a kan abin da ba za ku ƙoshi ba?
Ku saurara, ku saurare ni, ku kuma ci abin da yake da kyau,
ranku kuma zai ji daɗin abinci mafi kyau.
3 Ku kasa kunne ku kuma zo gare ni;
ku saurare ni, don ranku ya rayu.
Zan yi madawwamin alkawari da ku,
zan nuna muku ƙaunata marar ƙarewa da na yi wa Dawuda alkawari.
4 Duba, na mai da shi shaida ga mutane,
shugaba da kuma jagorar mutane.
5 Tabbatacce za ku kira al'umman da ba ku sani ba,
kuma al'umman da ba ku sani ba za su sheƙo a guje zuwa wurinku,
saboda UBANGIJI Allahnku,
Mai Tsarkin nan na Isra'ila,
gama ya darjanta ku."
6 Ku nemi UBANGIJI tun yana samuwa;
ku yi kira gare shi tun yana kusa.
7 Bari mugu ya bar irin halinsa
mugu kuma ya sāke irin tunaninsa.
Bari yă juyo ga UBANGIJI, zai kuwa ji tausayinsa,
ya juyo ga Allahnmu kuma, gama shi mai gafartawa ne a sauƙaƙe.

8 "Gama tunanina ba tunaninku ba ne,
yadda kuke yin abubuwa ba yadda nake yin abubuwa ba ne,"
in ji UBANGIJI.
9 "Kamar yadda sammai suke can nesa da ƙasa,
haka yadda nake yin abubuwa suke dabam da yadda kuke yin abubuwa
tunanina kuma dabam da naku.
10 Kamar yadda ruwan sama da dusar ƙanƙara suke
saukowa daga sama,
ba sa komowa
ba tare da sun jiƙe duniya
sun kuma sa su yi 'ya'ya su kuma yi toho,
don su ba da iri ga mai shuki da kuma abinci ga mai ci,
11 haka maganata da take fitowa daga bakina.
Ba za tă koma gare ni wofi ba,
amma za tă cika abin da nake so
ta kuma cika abin da na aike ta tă yi.
12 Za ku fita da farin ciki
a kuma bi da ku da salama;
duwatsu da tuddai
za su ɓarke da waƙa a gabanku,
dukan itatuwan jeji kuma
za su tafa hannuwansu.
13 A maimakon sarƙaƙƙiya, itacen fir ne zai tsiro,
a maimakon ƙayayyuwa kuma, itacen ci-zaƙi ne zai tsiro.
Wannan zai zama matuni na abin da Ni UBANGIJI na yi,
madawwamiyar alama ce,

wadda ba za a datse ba."

# 56

*Ceto domin waɗansu*

1 Ga abin da UBANGIJI yana cewa,
"Ku riƙe gaskiya
ku yi abin da yake daidai,
gama cetona yana kusa
za a kuma bayyana adalcina nan da nan.
2 Mai albarka ne mutumin da ya aikata wannan,
mutumin da ya riƙe kam
yana kiyaye Asabbaci ba tare da ƙazantar da shi ba,
yana kuma kiyaye kansa daga yin mugun abu."

3 Kada baƙon da ya miƙa kansa ga UBANGIJI ya ce,
"Ai UBANGIJI zai ware ni daga mutanensa."
Kada kuma wani bābā ya yi gunaguni cewa,
"Ni busasshen itace ne kawai."
4 Gama ga abin da UBANGIJI ya faɗa,
"Wa bābānnin da suna kiyaye Asabbatai,
waɗanda suka zaɓi yin abin da ya gamshe ni
suna kuma riƙe da alkawarina kankan,
5 a gare su cikin haikalina da kuma bangayensa
zan ba da matuni da kuma suna
mafi kyau fiye da 'ya'ya maza da kuma 'ya'ya mata;
zan ba su madawwamin sunan
da ba za a raba su da shi ba.
6 Baƙin da suka miƙa kansu ga UBANGIJI
don su bauta masa,
su kuma ƙaunaci sunan UBANGIJI,
waɗanda kuma suke yin masa sujada,
duk waɗanda suka kiyaye Asabbaci ba tare da ƙazantar da shi ba
suka kuma riƙe alkawarina kankan,
7 waɗannan ne zan kai tsattsarkan dutsena
in sa su yi farin ciki a gidana na addu'a.
Hadayunsu na ƙonawa da sadakokinsu
za su zama abin karɓa a bagadena;
gama za a ce da gidana
gidan addu'a domin dukan al'ummai."
8 UBANGIJI Mai Iko Duka ya furta cewa,
zai tattara korarru na Isra'ila,
"Zan ƙara tattaro waɗansu
bayan waɗanda na riga na tattara."

*Zargin da Allah ya yi a kan mugaye*

9 Ku zo, dukanku namun jeji,
ku zo ku ci, dukanku namun jeji!
10 Matsaran Isra'ila makafi ne,
dukansu jahilai ne;
dukansu bebayen karnuka ne
ba za su iya haushi ba;
suna kwance ne kawai suna mafarki,

suna son barci ba dama.
11 Su karnuka ne masu kwaɗayi;
ba su taɓa ƙoshi.
Su makiyaya ne marasa ganewa;
duk sun nufi inda suka ga dama,
kowa yana nemar wa kansa riba.
12 Kowanne yakan ce, “Zo, bari in samo ruwan inabi!
Bari mu cika cikinmu da barasa!
Gobe ma zai zama kamar yau,
ko ma fiye da haka.”

# 57

1 Mai adalci yakan mutu,
ba kuwa wanda yakan yi tunani a zuciyarsa;
an kwashe mutanen kirki,
ba kuwa wanda ya fahimta
cewa an kwashe masu adalci
don a tsame su daga mugunta.
2 Waɗanda suke aikata abin da yake daidai
sukan shiga da salama;
sukan huta yayinda suka kwanta cikin kabari.
3 “Amma ku, ku matso nan, ku ’ya’ya maza na masu sihiri,
ku zuriyar mazinata da karuwai!
4 Wane ne kuke yi wa ba’a?
Ga wa kuke masa gwalo
kuna kuma fitar da harshe?
Ashe, ku ba tarin ’yan tawaye ba ne,
zuriyar maƙaryata?
5 Kuna cike da muguwar sha’awa mai ƙonawa a cikin itatuwan oak
da kuma a ƙarƙashin kowane itace mai inuwa;
kuna miƙa hadayar ’ya’yanku a rafuffuka
da kuma a ƙarƙashin tsagaggun duwatsu.
6 Gumakan da suke cikin duwatsu masu sulɓi su ne rabonku;
su ɗin, su ne rabonku.
I, gare su kuka kwarara hadayu na sha
kuka kuma miƙa hadayu na gari.
Saboda waɗannan abubuwa, zan yi haƙuri?
7 Kun yi gadonku a dogayen duwatsu masu tsayi da kuma a tudu mai tsawo;
a can kuka haura don ku miƙa hadayunku.
8 A bayan ƙofofi da madogaran ƙofofi
kuka kafa alamun gumakanku.
Kuka yashe ni, kuka kware gadonku,
kuka kwanta a kansa kuka fadada shi;
kuka kuma ƙulla yarjejjeniya da waɗanda kuke ƙaunar gadajensu,
kuka dubi tsiraicinsu.
9 Kuka tafi wurin Molek* da man zaitun
kuka kuma riɓaɓɓanya turarenku.
Kuka aika jakadunku† can da nisa;
kuka gangara zuwa cikin kabari kansa!

* 57:9 Ko kuwa zuwa wurin sarki † 57:9 Ko kuwa gumakan

10 Kuka gaji cikin dukan al'amuranku,
amma ba ku iya cewa, 'Aikin banza ne ba.'
Kuka sami sabuntar ƙarfinku,
ta haka ba ku suma ba.

11 "Wa ya sa ku fargaba, kuna jin tsoro
har kuka yi mini ƙarya,
ba ku kuma tuna da ni ba
balle ku yi tunanin wannan a zukatanku?
Ba don na daɗe ina shiru ba ne
ya sa ba kwa tsorona?
12 Zan bayyana adalcinku da kuma ayyukanku,
ba kuwa za su amfane ku ba.
13 Sa'ad da kuka nemi taimako,
bari tarin gumakanku su cece ku!
Iska za tă kwashe dukansu tă tafi,
ɗan numfashi kawai zai hura su.
Amma mutumin da ya mai da ni mafakarsa
zai gāji ƙasar
ya kuma mallaki dutsena mai tsarki."

*Ta'aziyya don mai tuba*

14 Za a kuma ce,
"Ku gina, ku gina, ku gyara hanya!
Ku kawar da abubuwan sa tuntuɓe a hanyar mutanena."
15 Gama abin da Maɗaukaki da kuma Mai daraja ya faɗa
wanda yake raye har abada, wanda sunansa mai tsarki ne,
"Ina zama a bisa da kuma a tsattsarkan wuri,
amma kuma tare da shi wanda yake mai halin tuba mai tawali'u a ruhu,
don in farfaɗo da ruhu mai tawali'u
in kuma farfaɗo da zuciyar mai halin tuba.
16 Ba zan tuhume su har abada ba,
ba kuwa kullum zai yi fushi ba,
gama a haka ruhun mutumin zan yi suma a gabana,
shi numfashin mutumin da na halitta.
17 Na yi fushi saboda kwaɗayin zunubinsa;
na yi masa horo, na kuma ɓoye fuskata saboda fushi,
duk da haka ya ci gaba da ayyukan zunubinsa.
18 Na ga al'amuransa, amma zan warkar da shi;
zan bi da shi in mayar da ta'aziyya a gare shi,
19 ina ƙirƙiro yabo a leɓunan masu makoki a Isra'ila.
Salama, salama, ga waɗanda suke nesa da kuma kusa,"
in ji UBANGIJI. "Zan kuma warkar da su."
20 Amma mugaye suna kama da tumbatsar teku,
wanda ba ya natsuwa,
wanda raƙumansa sukan kawo gurɓacewa da tabo.
21 "Babu salama ga mugaye," in ji Allahna.

# 58

*Azumi na gaskiya*

1 "Ku yi ihu da ƙarfi, ba ƙaƙƙautawa.
Ku tā da muryarku kamar busar ƙaho.

Ku furta wa mutanena tawayensu
da kuma ga gidan Yaƙub zunubansu.
2 Gama kowace rana suna nemana;
suna marmarin sanin hanyoyina,
sai ka ce al'ummar da take yin abin da yake daidai
ba ta kuma yashe umarnan Allahnta ba.
Sun nemi shawarwaran da suke daidai daga gare ni
suna kuma marmari Allah ya zo kusa da su.
3 Suna cewa, 'Don me muka yi azumi,
ba ka kuma gani ba?
Me ya sa muka ƙasƙantar da kanmu,
ba ka kuma lura da wannan ba?'

"Duk da haka a ranar azuminku, kuna yi yadda kuka ga dama
kuna kuma zaluntar dukan ma'aikata.
4 Azuminku yakan ƙare a faɗa da kuma hargitsi,
kuna ta naushin juna da mugayen naushe-naushe.
Ba za ku iya azumi kamar yadda kuke yi a yau
ku zaci za a ji muryarku can sama.
5 Irin azumin da na zaɓa ke nan,
rana guda kawai don mutum ya ƙasƙantar da kansa?
Sunkuyar da kanku kamar iwa kawai
kuna kuma kwance a tsummoki da toka?
Abin da kuke kira azumi ke nan
rana yardajje ga UBANGIJI?

6 "Irin azumin da na zaɓa shi ne,
a kunce sarƙoƙin rashin adalci
a kuma kunce igiyoyin karkiya,
a 'yantar da waɗanda ake zalunta
a kuma kakkarye kowace karkiya?
7 Ba shi ne ku rarraba abincinku da mayunwata
ku kuma tanada wa matalauta masu yawo mahalli,
sa'ad da kuka ga wanda yake tsirara, ku yi masa sutura,
kada kuma ku ba wa namanku da jininku baya?
8 Sa'an nan haskenku zai keto kamar ketowar alfijir,
warkarwarku kuma zai bayyana nan da nan;
sa'an nan adalcinku* zai tafi a gabanku,
ɗaukakar UBANGIJI kuma zai tsare ku daga baya.
9 Sa'an nan za ku yi kira, UBANGIJI kuma zai amsa;
za ku yi kuka don neman taimako, zai kuwa ce ga ni nan.

"In kuka kawar da karkiyar zalunci,
kuka daina nuna wa juna yatsa da kuma faɗar mugayen maganganu,
10 in kuma kuka ɗauki lokaci kuka ƙosar da mayunwata
kuka kuma biya bukatun waɗanda suke shan tsanani,
sa'an nan ne haskenku zai haskaka cikin duhu
darenku kuma zai zama kamar tsakar rana.
11 UBANGIJI zai bishe ku kullum;
zai biya muku bukatunku a ƙasa mai zafin rana
ya kuma ƙarfafa ƙasusuwanku.

* **58:8** Ko kuwa Mai Adalcinka

Za ku zama kamar lambun da aka yi masa banruwa,
kamar rafin da ruwansa ba ya ƙafewa.
12 Mutanenku za su sāke gina kufai na da
su kuma daga tsofaffin harsashai;
za a ce da ku Masu Gyaran Katangar da ta Rushe,
Masu Farfaɗo da Trituna da kuma Wuraren zama.

13 “In kun kiyaye ƙafafunku daga take Asabbaci
da kuma daga aikata abin da kuka gan dama a ranata mai tsarki,
in kuka kira Asabbaci ranar murna
rana mai tsarki ta UBANGIJI kuma mai bangirma,
in kuka girmama ta ta wurin ƙin yin abin da kuka gan dama
da kuma yin al’amuranku ko yin mugayen maganganu,
14 sa’an nan za ku yi farin ciki a cikin UBANGIJI,
zan kuma sa ku a kan maɗaukaka ƙasashe
ku kuma yi biki a gādon mahaifinku Yaƙub.”
Ni UBANGIJI ne na faɗa.

# 59

*Zunubi, furci da kuma fansa*

1 Tabbatacce hannun UBANGIJI bai kāsa yin ceto ba,
kunnensa kuma bai kurmance da zai kāsa ji ba.
2 Amma laifofinku sun raba
ku da Allahnku;
zunubanku sun ɓoye fuskarsa daga gare ku,
saboda kada yǎ ji.
3 Gama hannuwanku sun ƙazantu da jini,
yatsotsinku kuma da alhaki.
Leɓunanku suna faɗin ƙarairayi,
harshenku kuma yana raɗar mugayen abubuwa.
4 Babu wani mai ce a yi adalci;
babu wani mai nema a dubi al’amarinsa da mutunci.
Sun dogara a gardandamin banza suna ƙarairayi;
suna ɗaukar cikin ɓarna, su haifi mugunta.
5 Suna ƙyanƙyashe ƙwan kāsā
su kuma saƙa yanar gizo-gizo.
Duk wanda ya ci ƙwansu zai mutu,
kuma sa’ad da ƙwan ya fashe, zai ƙyanƙyashe kububuwa.
6 Yanar gizo-gizonsu ba amfani don tufa;
ba za su iya rufuwa da abin da suka yi ba.
Ayyukansu mugaye ne,
ayyukan tā da hargitsi kuma suna a hannuwansu.
7 Kafafunsu sukan gaggauta zuwa aikata zunubi;
suna da saurin zub da jini.
Tunaninsu mugaye ne;
lalaci da hallaka sun shata hanyoyinsu.
8 Ba su san hanyar salama ba;
babu adalci a hanyoyinsu.
Sun mai da su karkatattun hanyoyi;
babu wanda zai yi tafiya a kansu ya sami salama.
9 Saboda haka gaskiya ta yi nisa da mu,

adalci kuma ba ya kaiwa gare mu.
Muna neman haske,
sai ga duhu;
muna neman haske, sai muka yi ta tafiya cikin baƙin inuwa.
10 Kamar makafi, sai lallubar bango muke yi,
muna lallubawar hanyarmu kamar marasa idanu.
Da tsakar rana muna tuntuɓe sai ka ce wuri ya fara duhu;
cikin ƙarfafa, mun zama kamar matattu.
11 Muna gurnani kamar beyar;
muna ta ƙugi kamar kurciyoyi.
Muna ta neman adalci amma ina;
mun nemi fansa, amma yana can da nisa.

12 Gama laifofinmu suna da yawa a gabanka,
zunubanmu kuma suna ba da shaida gāba da mu.
Laifofinmu kullum suna a gabanmu,
muna kuma sane da laifofinmu,
13 tawaye da mūsun UBANGIJI,
mun juye bayanmu ga Allahnmu,
zugawa a yi zalunci da tayarwa,
faɗin ƙarairayi da zukatanmu suka shirya.
14 Saboda haka aka kau da yin gaskiya
adalci kuma ya tsaya can da nesa;
gaskiya ta yi tuntuɓe a dituna,
sahihanci ba zai shiga ba.
15 Gaskiya ta ɓace gaba ɗaya,
kuma duk wanda ya guji mugunta zai zama ganima.

UBANGIJI ya duba bai kuwa ji daɗi
cewa babu adalci ba.
16 Ya ga cewa babu wani,
ya yi mamaki cewa babu wanda zai shiga tsakani;
saboda haka hannunsa ya aikata masa ceto,
adalcinsa kuma ya raya shi.
17 Ya yafa sulke a matsayin rigar ƙirji,
da hulan kwanon ceto a kansa;
ya sa rigunan ɗaukar fansa
ya kuma nannaɗe kansa da kishi kamar a cikin alkyabba.
18 Bisa ga abin da suka yi,
haka za a sāka
fushi a kan abokan gābansa
ramuwa kuma a kan maƙiyansa;
zai sāka wa tsibirai abin da ya dace da su.
19 Daga yamma, mutane za su ji tsoron UBANGIJI,
daga mafitar rana kuma, za su girmama ɗaukakarsa.
Gama zai zo kamar rigyawa mai tsananin gudu
cewa numfashin UBANGIJI zai tafi tare da shi.*

20 "Mai fansa zai zo Sihiyona,

* **59:19** Ko kuwa Sa'ad da abokin gāba ya shigo kamar rigyawa, Ruhun UBANGIJIzai kore shi.

zuwa waɗanda suke cikin Yaƙub da suka tuba daga zunubansu,"
in ji UBANGIJI.
21 "Game da ni dai, ga alkawarina da su," in ji UBANGIJI. "Ruhuna, wanda yake a
kanka, da kuma maganata da na sa a bakinka ba za tă rabu da bakinka ba, ko daga
bakunan 'ya'yanka ba, ko kuwa daga bakunan zuriyarsu ba daga wannan lokaci
zuwa gaba da kuma har abada," in ji UBANGIJI.

# 60

*Ɗaukakar Sihiyona*

1 "Ki tashi, ki haskaka, gama haskenki ya zo,
ɗaukakar UBANGIJI ya taso a kanki.
2 Duba, duhu ya rufe duniya
duhu mai kauri kuma yana bisa mutane,
amma UBANGIJI ya taso a kanki
ɗaukakarsa kuma ya bayyana a bisanki.
3 Al'ummai za su zo wurin haskenki,
sarakuna kuma zuwa asubahin sabon yininki.

4 "Ki ɗaga idanunki ki duba kewaye da ke.
Duka sun tattaru suka kuma zo wurinki;
'ya'yanki maza daga nesa,
ana kuma ɗaukan 'ya'yanki mata a hannu.
5 Sa'an nan za ki duba ki kuma haskaka
zuciyarki zai motsa ya kuma cika da farin ciki;
za a kawo miki wadata daga tekuna,
za a kawo miki arzikin al'ummai.
6 Manyan ayarin raƙuma za su cika ƙasar,
ƙananan raƙuma ke nan daga Midiyan da Efa.
Daga Sheba kuma duka za su zo,
suna ɗauke da zinariya da turare
suna shelar yabon UBANGIJI.
7 Dukan garkunan Kedar za su taru a wurinki
ragunan Nebayiwot za su yi miki hidima;
za a karɓe su kamar hadayu a kan bagadenki,
zan kuma darjanta haikalina mai ɗaukaka.

8 "Su wane ne waɗannan da suke firiya kamar gizagizai,
kamar kurciyoyi suna zuwa sheƙarsu?
9 Babu shakka tsibirai suna dogara gare ni;
jiragen Tarshish kuma su ne a gaba,
suna kawo 'ya'yanki maza daga nesa,
tare da azurfa da zinariya,
domin su girmama UBANGIJI Allahnki,
Mai Tsarkin nan na Isra'ila,
gama ya cika ki da daraja.

10 "Baƙi za su sāke gina katangarki,
sarakunansu kuma za su yi miki hidima.
Ko da yake a cikin fushi na buge ki,
da tagomashi zan yi miki jinƙai.

11 Kofofinki kullum za su kasance a buɗe,
ba za a ƙara rufe su da rana ko da dare ba,
saboda mutane su kawo miki dukiyar al'ummai,
sarakunansu za su kasance a gaba a jerin gwanon nasara.
12 Gama al'umma ko masarautar da ba tă bauta miki ba, za tă hallaka;
za tă lalace sarai.

13 "Darajar Lebanon za tă zo wurinki,
itatuwan fir da dai ire-irensu da kuma itatuwan saifires duka
za su zo don su ƙayatar da wurina mai tsarki;
zan kuma ɗaukaka wurin ƙafafuna.
14 'Ya'ya maza masu zaluntarku za su zo suna rusunawa a gabanki;
dukan waɗanda suka rena ki za su rusuna a ƙafafunki
su kuma ce da ke Birnin UBANGIJI,
Sihiyona na Mai Tsarkin nan na Isra'ila.

15 "Ko da yake an yashe ki aka kuma ƙi ki,
har babu wani da ya ratsa a cikinki,
zan mai da ke madawwamiyar abar taƙama
da kuma farin cikin dukan zamanai.
16 Za ki sha madarar al'ummai
a kuma shayar da ke da nonon sarauta.
Sa'an nan za ki san cewa ni, UBANGIJI, ni ne Mai Cetonki,
Mai Fansarki, Mai Ikon nan na Yaƙub.
17 A maimakon tagulla zan kawo zinariya,
azurfa kuma a maimakon baƙin ƙarfe.
A maimakon katako zan kawo tagulla,
baƙin ƙarfe kuma a maimakon duwatsu.
Zan sa salama ta zama gwamnarki
adalci kuma mai mulkinki.
18 Ba za a ƙara jin hayaniyar tashin hankali a ƙasarki ba,
balle lalacewa ko hallaka a cikin iyakokinki,
amma za ki kira katangarki Ceto
ƙofofinki kuma Yabo.
19 Rana ba za tă ƙara zama haskenki a yini ba,
balle hasken wata ya haskaka a kanki,
gama UBANGIJI zai zama madawwamin haskenki,
Allahnki kuma zai zama ɗaukakarki.
20 Ranarki ba za tă ƙara fāɗuwa ba
watanki kuma ba zai ƙara shuɗewa ba;
UBANGIJI zai zama madawwamin haskenki,
kwanakin baƙin cikinki za su ƙare.
21 Sa'an nan dukan mutanenki za su zama masu adalci
za su kuma mallaki ƙasar har abada.
Su ne reshen da na shuka,
aikin hannuwana,
don nuna darajata.
22 Mafi ƙanƙanta a cikinki za tă zama dubu,
ƙarami zai zama al'umma mai girma.
Ni ne UBANGIJI,
cikin lokacinsa zan yi haka da sauri."

# 61

*Shekarar tagomashin Ubangiji*

1 Ruhun Ubangiji Mai Iko Duka yana a kaina,
domin Ubangiji ya shafe ni
domin in yi wa'azi labari mai daɗi ga matalauta.
Ya aiko ni in warkar da waɗanda suka karai a zuci,
don in yi shelar 'yanci don ɗaurarru
in kuma kunce 'yan kurkuku daga duhu
2 don in yi shelar shekarar tagomashin Ubangiji
da kuma ranar ɗaukan fansar Allahnmu,
don in ta'azantar da dukan waɗanda suke makoki,
3 in tanada wa waɗanda suke baƙin ciki a Sihiyona,
in maido musu rawani mai kyau
a maimako na toka,
man murna
a maimako na makoki,
da kuma rigar yabo
a maimako na ruhun fid da zuciya.
Za a ce da su itatuwan oak na adalci,
shukin Ubangiji
don bayyana darajarsa.
4 Za su sāke gina kufai na dā
su raya wurare da aka lalace tun da daɗewa;
za su sabunta biranen da aka rurrushe
da aka lalace tun zamanai masu yawa da suka wuce.
5 Baƙi za su yi kiwon garkunanki;
baƙi za su yi miki noman gonaki da gonakin inabinki.
6 Za a kuma kira ku firistocin Ubangiji,
za a kira ku masu hidimar Allahnmu.
Za ku ci wadatar waɗansu al'ummai,
kuma a cikin dukiyarsu za ku yi taƙama.

7 A maimakon kunyarsu
mutanena za su sami rabi riɓi biyu,
a maimakon wulaƙanci
za su yi farin ciki cikin gādonsu;
ta haka za su gāji rabo riɓi biyu a ƙasarsu,
da kuma madawwamin farin ciki zai zama nasu.

8 "Gama ni, Ubangiji, ina ƙaunar adalci;
na ƙi fashi da aikata laifi.
Cikin adalcina zan sāka musu
in kuma yi madawwamin alkawari da su.
9 Za a san da zuriyarsu a cikin al'ummai
'ya'yansu kuma a cikin mutane.
Dukan waɗanda suka gan su za su san
cewa su mutane ne da Ubangiji ya sa wa albarka."

10 Ina jin daɗi ƙwarai a cikin Ubangiji;
raina yana farin ciki a cikin Allahna.
Gama ya suturce ni da rigunan ceto
ya yi mini ado da rigar adalci,

yadda ango yakan yi wa kansa ado kamar firist
kamar kuma yadda amarya takan sha ado da duwatsunta masu daraja.
11 Gama kamar yadda ƙasa takan sa tsire-tsire su tohu
lambu kuma ya sa iri ya yi girma,
haka UBANGIJI Mai Iko Duka zai sa adalci da yabo
su tsiro a gaban dukan al'ummai.

# 62

*Sabon sunan Sihiyona*

1 Saboda Sihiyona ba zan yi shiru ba,
saboda Urushalima ba zan huta ba,
sai adalcinta ya haskaka kamar hasken safiya,
cetonta kuma ya haskaka kamar fitila mai haske.
2 Al'ummai za su ga adalcinki,
sarakuna kuma za su ga ɗaukakarki;
za a kira ki da sabon suna
sunan da bakin UBANGIJI zai ambata.
3 Za ki zama rawanin daraja a hannun UBANGIJI,
rawanin sarauta a hannun Allahnki.
4 Ba za a ƙara ce da ke Yasasshiya ba,
ko a kira ƙasarki Kango.
Amma za a ce da ke Hefziba*
ƙasarki kuma Bewula;†
gama UBANGIJI zai ji daɗinki,
ƙasarki kuma za tă yi aure.
5 Kamar yadda saurayi kan auri yarinya,
haka 'ya'yanki maza‡ za su aure ki;
kamar kuma yadda ango yakan yi farin ciki da amaryarsa,
haka Allahnki zai yi farin ciki da ke.
6 Na sa matsara a kan katangarki, ya Urushalima;
ba za su taɓa yin shiru ba, dare da rana.
Ku da kuke kira bisa sunan UBANGIJI,
kada ku ba kanku hutu,
7 kuma kada ku ba shi hutu sai ya kafa Urushalima
ya kuma mai da ita yabon duniya.

8 UBANGIJI ya rantse da hannunsa na dama
ta hannunsa kuma mai iko cewa,
"Ba zan ƙara ba da hatsinki
ya zama abinci ga abokan gābanki ba,
baƙi kuma ba za su ƙara shan ruwan inabin
wanda kika sha wahala samu ba;
9 amma waɗanda suka girbe shi za su ci shi
su kuma yabi UBANGIJI,
waɗanda kuma suka tattara 'ya'yan inabi za su sha shi
a filayen wurina mai tsarki."

10 Ku wuce, ku wuce ƙofofi!
Ku shirya hanya saboda mutane.

* **62:4** Hefziba yana nufin farin cikina yana a cikinta. † **62:4** Bewula yana nufin wadda ta yi aure. ‡ **62:5** Ko kuwa Mai gini

Ku gina, ku gina babbar hanya!
Ku kawar da duwatsu.
Ku ɗaga tuta saboda al'ummai.

11 UBANGIJI ya yi shela
ga iyakokin duniya cewa,
"Faɗa wa Diyar Sihiyona,
'Ga Mai Cetonki yana zuwa!
Ga ladarsa tana tare da shi,
sakamakonsa yana raka shi.' "
12 Za a ce da shi Tsattsarkar Mutane,
Fansassu na UBANGIJI;
za a kuma ce da ke Wadda Aka Nema
Birnin da Ba Za a Kara Yashe ta ba.

# 63

*Ranar ɗaukan fansa da kuma ceto na Allah*

1 Wane ne wannan mai zuwa daga Edom,
daga Bozra, saye da jajjayen rigunarsa?
Wane ne wannan, sanye cikin daraja,
tafe cikin girmar ƙarfinsa?
"Ni ne, mai magana cikin adalci,
mai ikon ceto."

2 Me ya sa rigunanka suka yi ja,
sai ka ce na wanda yake tattaka 'ya'yan inabi?

3 "Na tattake 'ya'yan inabi ni kaɗai;
cikin al'ummai kuma babu wani tare da ni.
Na tattake su cikin fushina
Na matse su cikin hasalata;
jininsu ya fantsamar wa rigunana,
na kuma ɓata dukan tufafina.
4 Gama ranar ɗaukan fansa tana a cikin zuciyata,
kuma shekarar fansata ta zo.
5 Na duba, amma babu wanda zai taimaka,
na yi mamaki cewa ba wanda ya goyi baya;
saboda haka hannuna ya yi mini ceto,
fushina kuma ya rayar da ni.
6 Na tattake al'ummai cikin fushina;
cikin hasalata kuma na sa sun bugu
na kuma zub da jininsu a ƙasa."

*Yabo da addu'a*

7 Zan ba da labarin alherin UBANGIJI,
ayyukan da suka sa a yabe shi,
bisa ga dukan abubuwan da UBANGIJI ya yi mana,
I, ayyuka masu kyan da ya yi
domin gidan Isra'ila,
bisa ga jinƙansa da yawan alheransa.
8 Ya ce, "Babu shakka su mutanena ne,
'ya'ya maza waɗanda ba za su ruɗe ni ba";
ta haka ya zama Mai Cetonsu.

9 Cikin dukan damuwarsu shi ma ya damu,
mala'ikan da yake gabansa ya cece su.
Cikin ƙauna da jinƙai ya fanshe su;
ya kuma ɗaga su ya riƙe su
dukan kwanakin dā
10 Duk da haka suka yi tawaye
suka ɓata wa Ruhu Mai Tsarki rai.
Saboda haka ya juya ya kuma zama abokin gābansu
shi kansa kuma ya yaƙe su.

11 Sa'an nan mutanensa suka tuna* kwanakin dā,
kwanakin Musa da mutanensa,
ina yake shi wanda ya fitar da su ta teku,
da makiyayan garkensa?
Ina shi yake wanda ya sa
Ruhunsa Mai Tsarki a cikinsu,
12 wanda ya aika hannu ɗaukakarsa mai iko
ya kasance a hannun dama na Musa,
wanda ya raba ruwaye a gabansu,
don yă sami wa kansa madawwamin suna,
13 wanda ya bishe su cikin zurfafa?
Kamar doki a fili,
ba su yi tuntuɓe ba;
14 kamar shanun da suke gangarawa zuwa kwari,
haka Ruhun UBANGIJI ya ba su hutu.
Ga yadda ka bishe mutanenka
don ka ba wa kanka suna mai ɗaukaka.

15 Ka duba daga sama ka gani
daga kursiyinka da yake bisa, mai tsarki da kuma mai ɗaukaka.
Ina kishinka da kuma ikonka?
Ka janye juyayi da kuma tausayin da kake yi mana daga gare mu.
16 Amma kai Ubanmu ne,
ko Ibrahim bai san mu ba
Isra'ila kuma bai yarda da mu ba;
kai, ya UBANGIJI, kai ne Ubanmu,
Mai Fansarmu tun fil azal ne sunanka.
17 Don me, ya UBANGIJI, ka sa muna barin hanyoyinka
muka kuma taurare zukatanmu don kada mu girmama ka?
Ka komo domin darajar bayinka,
kabilan da suke abin gādonka.
18 Gama a ɗan lokaci mutanenka suka mallaki wurinka mai tsarki,
amma yanzu abokan gābanmu sun tattake wurinka mai tsarki.
19 Mu naka tun fil azal;
ba ka taɓa yin mulki a kansu ba,
ba a taɓa kira su da sunanka ba.†

---

* **63:11** Ko kuwa Amma bari yă tuna † **63:19** Ko kuwa Mun zama kamar waɗanda ba ka taɓa yin mulkinsu ba, kamar waɗanda ba a taɓa kira da sunanka ba

# 64

1 Da ma za ka tsage sammai ka sauko,
ai, da duwatsu za su yi rawar jiki a gabanka!
2 Kamar sa'ad da wuta takan ci rassa
ta sa ruwa ya tafasa,
ka sauko ka sanar da sunanka ga abokan gābanka
ka kuma sa al'ummai su yi rawan jiki a gabanka!
3 Gama sa'ad da ka aikata abubuwan bantsoron da ba mu sa tsammani ba,
ka sauko, duwatsu kuma suka yi rawar jiki a gabanka.
4 Tun fil azal babu wanda ya taɓa ji,
babu kunnen da ya gane,
babu idon da ya ga wani Allah in ban da kai,
wanda ya aikata waɗannan al'amura a madadin waɗanda suke sa zuciya a gare shi.
5 Kakan taimaki waɗanda suke murnan yin abin da yake daidai,
waɗanda sukan tuna da hanyoyinka.
Amma sa'ad da muka ci gaba da yin zunubi,
kakan yi fushi.
Ta yaya za mu sami ceto ke nan?
6 Dukanmu mun zama kamar wanda yake marar tsabta,
kuma dukan ayyukanmu masu adalci sun zama kamar ƙazaman tsummoki;
duk mun zama kamar busasshen ganye,
kamar iska haka zunubanmu sukan share mu.
7 Babu wanda yake kira bisa sunanka
ko ya yi ƙoƙarin riƙe ka;
gama ka ɓoye fuskarka daga gare mu
ka kuma sa muka lalace saboda zunubanmu.
8 Duk da haka, UBANGIJI, kai ne Ubanmu.
Mu yumɓu ne, kai kuma mai ginin tukwane;
dukanmu aikin hannunka ne.
9 Kada ka yi fushi fiye da kima, ya UBANGIJI;
kada ka tuna da zunubanmu har abada.
Da ma ka dube mu, muna roƙonka,
gama dukanmu mutanenka ne.
10 Biranenka masu tsarki sun zama hamada;
har Sihiyona ma ta zama hamada; Urushalima ta zama kango.
11 Haikalinmu mai tsarki da kuma mai daraja, inda kakanninmu suka yabe ka,
an ƙone da wuta,
kuma dukan abubuwan da muke ƙauna sun lalace.
12 Bayan dukan wannan, ya UBANGIJI, ba za ka yi wani abu ba?
Za ka yi shiru ka hore mu fiye da kima?

# 65

*Hukunci da kuma ceto*

1 "Na bayyana kaina ga waɗanda ba su tambaye ni ba;
ina samuwa ga waɗanda ba su neme ni ba.
Ga al'ummar da ba tă kira bisa sunana ba,
Na ce, 'Ga ni, ga ni.'
2 Dukan yini ina miƙa hannuwana
ga mutane masu tayarwa,
waɗanda suna tafiya a hanyoyin da ba su da kyau,
suna bin tunaninsu,

3 mutanen da suna cin gaba da tsokanata
a fuskata,
suna miƙa hadayu a gonaki
suna ƙone turare a bagadan tubali;
4 suna zama a kaburbura
su kwana suna yin asirtattun ayyuka;
suna cin naman aladu,
tukwanensu kuma sun cika da nama marar tsabta;
5 suna cewa, ‘Ku tsaya a can; kada ku yi kusa da ni,
gama na fi ku tsarki!’
Irin mutanen nan hayaƙi ne a hancina,
wuta kuma da take cin gaba da ci dukan yini.

6 “Ga shi, yana nan a rubuce a gabana cewa
ba zan ƙyale ba, zan yi cikakken ramuwa;
zan yi ramuwa a cinyoyinsu
7 saboda zunubanku da kuma zunuban kakanninku,”
in ji UBANGIJI.
“Gama sun ƙone turare a kan duwatsu
suka kuma ƙazantar da ni a kan tuddai,
zan yi musu awo in zuba a cinyoyinsu
cikakken ramuwa saboda ayyukansu na dā.”
8 Ga abin da UBANGIJI yana cewa,
“Kamar sa’ad da ruwan ’ya’yan itace yana samuwa a cikin tarin ’ya’yan inabi
mutane kuma su ce, ‘Kada a lalace shi,
har yanzu akwai abu mai kyau a ciki,’
haka nan zan yi a madadin bayina;
ba zan hallaka su duka ba.
9 Zan fitar da zuriyar Yaƙub,
daga Yahuda kuma waɗanda za su mallaki duwatsuna;
zaɓaɓɓun mutanena za su gāje su,
a can kuma bayina za su zauna.
10 Sharon zai zama wurin kiwo don shanu,
Kwarin Akor kuma wurin hutun garkuna,
domin mutanena da suke nemana.

11 “Amma game da ku waɗanda kuka yashe UBANGIJI
kuka manta da dutsena mai tsarki kuwa,
ku da kuka shimfiɗa tebur don sa’a
kuka kuma cika darunan ruwan inabin da aka dama don Kaddara,
12 zan ƙaddara ku ga kaifin takobi,
dukanku kuma za ku sunkuya wa mai yanka;
gama na yi kira amma ba ku amsa ba,
na yi magana amma ba ku saurara ba.
Kuka aikata mugunta a gabana
kuka kuma zaɓi abin da ba na jin daɗi.”
13 Saboda haka ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa,
“Bayin za su ci,
amma ku za ku ji yunwa;
bayina za su sha,
amma ku za ku ji ƙishi;
bayina za su yi farin ciki

amma ku za ku sha kunya.
14 Bayina za su rera
da farin cikin zukatansu,
amma ku za ku yi kuka
daga wahalar zuciya
ku kuma yi kururuwa da karayar zuci.
15 Za ku bar sunanku
ga zaɓaɓɓuna yă zama abin la'antarwa;
UBANGIJI Mai Iko Duka zai kashe ku,
amma ga bayina zai ba su wani suna.
16 Duk wanda zai roƙi albarka a cikin ƙasar
zai yi haka da gaskiyar Allah;
wanda zai yi rantsuwa a cikin ƙasar
zai rantse da gaskiyar Allah.
Gama za a manta da wahalolin baya
a kuma ɓoye su daga idanuna.

### *Sabuwar sama da kuma sabuwar duniya*

17 "Ga shi, na halicci
sabuwar sama da kuma sabuwar duniya.
Abubuwa na dā za a manta da su,
ba kuwa za a ƙara tuna da su ba.
18 Amma ku yi murna ku kuma yi farin ciki har abada
a abin da na halitta,
gama zan halicci Urushalima ta zama abin murna
mutanenta kuwa abin farin ciki.
19 Zan yi farin ciki a kan Urushalima
in kuma yi murna saboda mutanena;
a can ba za a ƙara jin
karar makoki da na kuka ba.

20 "A cikinta ba za a ƙara jin
jariri ya rayu na 'yan kwanaki kawai ba,
ko kuwa wani tsohon da bai cika kwanakinsa ba;
duk wanda ya mutu yana da shekaru ɗari
za a ce ya mutu a kurciya ne kawai;
duk wanda bai kai* ɗari ba
za a ɗauka la'antacce ne.
21 Za su gina gidaje su kuma zauna a cikinsu;
za su yi shuki a gonakin inabi su kuma ci 'ya'yansu.
22 Ba za su ƙara gina gidaje waɗansu kuma su zauna a cikinsu ba,
ko su yi shuki waɗansu kuma su ci ba.
Gama kamar yadda kwanakin itace suke,
haka kwanakin mutanena za su kasance;
zaɓaɓɓuna za su daɗe suna jin daɗin
ayyukan hannuwansu.
23 Ba za su yi wahala a banza ba
ko su haifi 'ya'yan da aka ƙaddara da rashin sa'a;
gama za su zama mutanen da UBANGIJI ya yi wa albarka,
su da zuriyarsu tare da su.
24 Kafin su yi kira zan amsa;

---

* **65:20** Ko kuwa / mai zunubin da ya kai

yayinda suke cikin magana zan ji.
25 Kyarketai da ’yan raguna za su ci abinci tare,
zaki kuma zai ci buɗu kamar yadda shanu suke yi,
amma ƙura ce za tă zama abincin maciji.
Ba za su ƙara cuci ko su yi ɓarna
a kan dukan dutsena mai tsarki ba,”
in ji UBANGIJI.

## 66

*Hukunci da kuma bege*

1 Ga abin da UBANGIJI yana cewa,
“Sama kursiyina ce,
duniya kuma matashin sawuna.
Ina gidan da za ku gina mini?
Ina wurin hutuna zai kasance?
2 Ba hannuna ba ne ya yi dukan waɗannan abubuwa,
ta haka suka kasance?”
In ji UBANGIJI.

“Wannan mutum ne nake jin daɗi,
shi da yake mai ƙasƙanci da kuma zuciyar yin tuba,
yana kuma rawar jiki ga maganata.
3 Amma duk ya miƙa hadayar bijimi
yana kama da wanda ya kashe mutum,
kuma duk wanda ya miƙa ɗan rago,
kamar wanda ya karye wuyan kare;
duk wanda ya miƙa hadaya ta gari
yana kama da wanda ya yi sadakar jinin alade,
kuma duk wanda ya ƙone turaren tuni,
kamar wanda yake bauta gunki ne.
Sun zaɓi hanyoyinsu,
rayukansu kuma suna jin daɗin abubuwan banƙyamarsu;
4 saboda haka ni ma zan aukar musu da masifa mai zafi
in kuma kawo musu abin da suke tsoro.
Gama sa’ad da na yi kira, ba wanda ya amsa,
sa’ad da na yi magana, ba wanda ya saurara,
Sun aikata mugunta a idona
suka kuma zaɓa abin da ba na jin daɗi.”

5 Ku ji maganar UBANGIJI,
ku da kuke rawar jiki ga maganarsa,
“’Yan’uwanku da suke ƙinku,
suna kuma ware ku saboda sunana, sun ce,
‘Bari a ɗaukaka UBANGIJI,
don mu ga farin cikinku!’
Duk da haka za su sha kunya.
6 Ku ji wannan hayaniya daga birni,
ku ji surutu daga haikali!
Amon UBANGIJI ne
yana sāka wa abokan gābansa abin da ya dace da su.

7 “Kafin naƙuda ya fara mata,
ta haihu;
kafin zafi ya zo mata,
ta haifi ɗa.
8 Wa ya taɓa jin irin wannan abu?
Wa ya taɓa gani irin abubuwan nan?
Za a iya ƙirƙiro ƙasa a rana ɗaya
ko a haifi al’umma farat ɗaya?
Duk da haka da zarar Sihiyona ta fara naƙuda
sai ta haifi ’ya’yanta.
9 Zan kai mace har haihuwa
in kuma sa ta kāsa haihu?” In ji UBANGIJI.
“Zan rufe mahaihuwa
sa’ad da lokacin haihuwa ya yi?” In ji Allahnku.
10 “Ku yi farin ciki tare da Urushalima ku kuma yi murna saboda ita,
dukanku waɗanda kuke ƙaunarta;
ku yi farin ciki matuƙa tare da ita,
dukanku waɗanda kuke makoki a kanta.
11 Gama za ku tsotsa ku kuma ƙoshi
da nonon ta’aziyyarta;
za ku sha sosai
ku kuma ji daɗin yalwarta.”
12 Gama ga abin da UBANGIJI ya faɗa,
“Zan fadada salama gare ta kamar kogi,
wadatar al’ummai kuma kamar rafi mai gudu;
za ku tsotsa a kuma riƙe ku a hannunta
ku kuma yi wasa a gwiwoyinta.
13 Kamar yadda uwa takan ta’azantar da ɗanta
haka zan ta’azantar da ku;
za ku kuma ta’azantu a Urushalima.”

14 Sa’ad da kuka ga wannan, zuciyarku za tă yi farin ciki
za ku kuma haɓaka kamar ciyawa;
za a sanar da hannun UBANGIJI ga bayinsa,
amma za a nuna wa maƙiyansa fushinsa.
15 Ga shi, UBANGIJI yana zuwa da wuta,
kuma kekunan yaƙinsa suna kama da guguwa;
zai sauko da fushinsa da zafi,
tsawatawarsa kuma da harsunan wuta.
16 Gama da wuta da kuma takobi
UBANGIJI zai yi hukunci a kan dukan mutane,
kuma yawanci za su kasance waɗanda UBANGIJI zai kashe.

17 “Waɗanda suka tsarkake suka kuma tsabtacce kansu don su je lambu, suna bin
wannan da yake tsakiya* waɗannan da suke cin naman aladu da ɓeraye da waɗansu
abubuwan banƙyama, za su sadu da ƙarshensu tare,” in ji UBANGIJI.

18 “Ni kuwa, saboda ayyukansu da kuma tunaninsu, ina dab da zuwa in tattara
dukan al’ummai da harsuna, za su kuma zo su ga ɗaukakata.

19 “Zan kafa alama a cikinsu, zan kuma aika waɗansu da suka tsira zuwa al’ummai,
zuwa Tarshish, zuwa Libiya da Lidiya (sanannun ’yan aika), zuwa Tubal da kuma
Girka, da kuma zuwa manisantan tsibirai da ba su taɓa jin labarin sunana ba ko su
ga ɗaukakata. Za su yi shelar ɗaukakata a cikin al’ummai. 20 Za su kuma dawo da

* **66:17** Ko kuwa lambu a bayan wannan na masujadanku, kuma

dukan ʼyanʼuwanku, daga dukan alʼummai, zuwa dutsena mai tsarki a Urushalima
kamar hadaya ga UBANGIJI, a kan dawakai, a kekunan yaƙi da wagonu, da kuma a kan
alfadarai da kuma raƙuma,” in ji UBANGIJI. “Za su kawo su, kamar yadda Israʼilawa
suke kawo hadayun hatsi, zuwa haikalin UBANGIJI a cikin tsabtatattun kore. 21 Zan
kuwa zaɓa waɗansunsu kuma su zama firistoci da Lawiyawa,” in ji UBANGIJI.
22 “Kamar yadda sabuwar duniya da sabuwar sama za su tabbata a gabana,” in ji
UBANGIJI, “haka sunanku da zuriyarku za su tabbata. 23 Daga wannan sabon wata
zuwa wancan, kuma daga wannan Asabbaci zuwa wancan, dukan mutane za su zo
su rusuna a gabana,” in ji UBANGIJI. 24 “Za su kuma fita su ga gawawwakin mutanen
da suka yi mini tayarwa; tsutsotsin da suke cinsu ba za su taɓa mutuwa ba, balle
wutar da take ƙona su ta mutu, za su kuma zama abin ƙyama ga dukan mutane.”

# Irmiya

1 Kalmomin Irmiya ɗan Hilkiya, ɗaya daga cikin firistoci a Anatot a yankin
Benyamin. 2 Maganar Ubangiji ta zo gare shi a shekara ta goma sha uku ta sarautar
Yosiya ɗan Amon sarkin Yahuda, 3 da kuma a zamanin Yehohiyakim ɗan Yosiya sarkin
Yahuda, har zuwa watan biyar na shekara goma sha ɗaya na Zedekiya ɗan Yosiya
sarkin Yahuda, sa'ad da aka kai mutanen Urushalima zaman bauta.

*Kiran Irmiya*

4 Maganar Ubangiji ta zo mini cewa,

5 "Kafin in siffanta ka a cikin ciki na san* ka,
kafin a haife ka, na keɓe ka;
na naɗa ka ka zama annabi ga al'ummai."

6 Sai na ce, "Kayya, Ubangiji Mai Iko Duka, ban iya magana ba; ni ɗan yaro ne
kawai."

7 Amma Ubangiji ya ce mini, "Kada ka ce, 'Ni ɗan yaro ne kawai.' Dole ka je wurin
kowane mutumin da na aike ka ka kuma faɗa abin da na umarce ka. 8 Kada ka ji
tsoronsu, gama ina tare da kai kuma zan kiyaye ka," in ji Ubangiji.

9 Sai Ubangiji ya miƙa hannunsa ya taɓa bakina ya ce mini, "Yanzu na sa
kalmomina a bakinka. 10 Duba, yau na naɗa ka a kan al'ummai da mulkoki don
ka tumɓuke ka kuma rusar, ka hallaka ka kuma kakkaɓe, ka gina ka kuma shuka."

11 Maganar Ubangiji ta zo mini cewa, "Me ka gani, Irmiya?"

Sai na amsa na ce, "Na ga reshen itacen almon."

12 Ubangiji ya ce mini, "Daidai ne ka gani, gama ina lura in ga cewa maganata ta
cika."

13 Maganar Ubangiji ta sāke zo mini cewa, "Me ka gani?"

Na amsa na ce, "Na ga tukunya tana tafasa, tana juyewa daga arewa."

14 Ubangiji ya ce mini, "Daga arewa za a zubo masifa a kan dukan mazaunan ƙasar.
15 Ina shirin kiran dukan mutanen masarautar arewanci," in ji Ubangiji.
"Sarakunansu za su zo su kafa kursiyoyinsu
a mashigin ƙofofin Urushalima;
za su zo su kewaye dukan katangarta
su kewaye dukan garuruwan Yahuda.
16 Zan furta hukunci a kan mutanena
saboda muguntarsu na yashe ni,
suna ƙona turare ga waɗansu alloli
suna kuma bauta wa abin da hannuwansu suka yi.

17 "Ka kintsa kanka! Ka tashi tsaye ka faɗa musu abin da na umarce ka. Kada su
firgita ka, in ba haka ba zan firgita ka a gabansu. 18 Yau na mai da kai birni mai
katanga, ginshiƙin ƙarfe da bangon tagulla don ka tsaya gāba da dukan ƙasar, ya
kuma yi gāba da sarakunan Yahuda da fadawan, da firistoci da kuma mutanenta.
19 Za su yi yaƙi da kai amma ba za su ci nasara a kanka ba, gama ina tare da kai, zan
kuma kiyaye ka," in ji Ubangiji.

## 2

*Isra'ila ya yashe Allah*

* **1:5** Ko kuwa zaɓe

1 Maganar UBANGIJI ta zo mini cewa, 2 “Tafi ka yi shela a kunnuwar Urushalima
cewa,
“ ‘Na tuna da amincin ƙuruciyarki,
yadda kamar amarya kika ƙaunace ni
kika kuma bi ni cikin hamada,
cikin ƙasar da ba a yi shuka ba.
3 Isra’ila tsattsarka ce ga UBANGIJI,
nunan fari na girbinsa;
dukan waɗanda suka cinye ta an same su da laifi,
masifa kuwa ta same su,’ ”
in ji UBANGIJI.

4 Ka saurari maganar UBANGIJI, ya gidan Yaƙub,
dukanku zuriyar gidan Isra’ila.
5 Ga abin da UBANGIJI yana cewa,
“Wane laifi ne kakanninku sun same ni da shi,
da suka tsaya nesa da ni?
Sun bi gumakan banza
su kansu suka kuma zama banza da kansu.
6 Ba su yi tambaya, ‘Ina UBANGIJI,
wanda ya fitar da su daga Masar
ya bishe su cikin jeji
cikin hamada da kwazazzabai
ƙasa mai fări da kuma duhu,
ƙasar da ba kowa mai ratsa ta ba kowa kuma mai zama a cikinta?’
7 Na kawo ku zuwa ƙasa mai albarka
don ku ci amfaninta da abubuwa masu yalwar da take bayarwa.
Amma kuka zo kuka ƙazantar da ƙasata
kuka kuma mai da gādona abin ƙyama.
8 Firistoci ba su yi tambaya,
‘Ina UBANGIJI ba.’
Waɗanda suke amfani da doka ba su san ni ba;
shugabanni suka yi mini tawaye.
Annabawa suka yi annabci ta wurin Ba’al,
suna bin gumakan banza.

9 “Saboda haka ina sāke tuhumarku,”
in ji UBANGIJI.
“Zan kuma tuhumi ’ya’ya ’ya’yanku.
10 Ku ƙetare zuwa tsibiran Kittim* ku gani,
ku aika zuwa Kedar ku duba da kyau;
ku ga ko an taɓa yin wani abu haka.
11 Akwai wata al’ummar da ta canja allolinta?
(Duk da haka su ba alloli ba ne sam.)
Amma mutanena sun musayar da ɗaukakarsu
da gumakan banza.
12 Ku girgiza saboda wannan, ya sammai,
ku kuma razana don tsoro mai girma,”
in ji UBANGIJI.
13 “Mutanena sun aikata zunubai guda biyu.
Sun rabu da ni,

* **2:10** Wato, Saifurus da tsibiran wajen yamma

ni da nake maɓulɓular ruwan rai,
sun kuma haƙa tankunan ruwansu,
tankuna ruwan da suka fashe da ba za su iya riƙe ruwa ba.
14 Isra'ila bawa ne, bawa ne ta wurin haihuwa?
Me ya sa ya zama ganima?
15 Zakoki sun yi ruri;
sun yi masa ruri.
Sun lalatar da ƙasarsa;
an ƙone garuruwansa aka kuma watse daga ciki.
16 Haka ma, mutanen Memfis† da Tafanes
sun aske rawanin kanka‡
17 Ba kai ne ba ka jawo wa kanka ba
ta wurin rabuwa da UBANGIJI Allahnka
sa'ad da ya bi da kai a hanya?
18 To, me ya sa za ka Masar
don shan ruwa daga Shihor?§
Kuma me ya sa za ka Assuriya
don shan ruwa daga Kogi?*
19 Muguntarka za tă hukunta ka;
jan bayanka zai tsawata maka.
Sai ka lura ka kuma gane
yaya mugu da kuma ɗaci suke a gare ka
sa'ad da ka rabu da UBANGIJI Allahnka
kuma ba ka tsorona,"
in ji UBANGIJI Maɗaukaki.

20 "Tun da daɗewa ka karya karkiyarka
ka kuma tsintsinke sarƙoƙinka;
sai ka ce, 'Ba zan bauta maka ba!'
Tabbatacce, a kan kowane tudu mai tsayi
da kuma a ƙarƙashin kowane ɗanyen itace
ka kwanta kamar karuwa.
21 Na shuka ka kamar zaɓaɓɓen inabi
iri mai kyau da kuma wanda za a dogara a kai.
Yaya kuma ka juya kana gāba da ni
ka lalace, ka zama inabin jeji?
22 Ko da yake ka wanke kanka da sabulu
ka yi amfani da sabulu mai yawa,
duk da haka har yanzu tabon laifinka yana nan a gabana,"
in ji UBANGIJI Mai Iko Duka.

23 "Yaya za ka ce, 'Ban ƙazantu ba;
ban bi Ba'al ba'?
Duba yadda ka yi a cikin kwari;
ka ga abin da ka yi.
Kai kamar makwaɗaciyar raƙuma ce mai zafin gudu
kana gudu nan da can,
24 kamar jakar jejin da ta saba da hamada,
mai busar iska cikin son barbaranta
sa'ad da take son barbara wa zai iya hana ta?

† **2:16** Da Ibraniyanci Nof ‡ **2:16** Ko kuwa fasa ƙoƙon kansa § **2:18** Wato, reshen Nilu * **2:18** Wato, Yuferites

Jakin da yake nemanta, ba ya bukatar wahalar da kansa;
a lokacin barbara za a same ta.
25 Kada ka yi gudu har ƙafafunka su zama ba takalma
maƙogwaronka kuma ya bushe.
Amma sai ka ce, ‘Ba amfani!
Ina ƙaunar baƙin alloli
kuma dole in bi su.’

26 “Kamar yadda akan kunyatar da ɓarawo sa’ad da aka kama shi,
haka gidan Isra’ila zai sha kunya,
su, sarakunansu da shugabanninsu,
firistocinsu da kuma annabawansu.
27 Kuna ce wa itace, ‘Kai ne mahaifina,’
ga dutse kuma, ‘Kai ne ka haife ni.’
Sun juye mini bayansu
ba fuskokinsu ba;
duk da haka sa’ad da suna cikin wahala, sukan ce,
‘Zo ka cece mu!’
28 To ina allolin da kuka yi wa kanku?
Bari su zo in suna iya cetonku
sa’ad da kuke cikin wahala!
Gama kuna da alloli masu yawa
kamar yadda kuke da garuruwa, ya Yahuda.

29 “Me ya sa kuke tuhumana?
Dukanku kun yi mini tawaye,”
in ji UBANGIJI.
30 “A banza na hukunta mutanenku;
ba su yi gyara ba.
Takobinku ya cinye annabawanku
kamar zaki mai jin yunwa.
31 “Ku na wannan zamani, ku saurari maganar UBANGIJI.
“Na zama wa Isra’ila hamada ne
ko ƙasa mai babban duhu?
Me ya sa mutanena suke cewa, ‘Muna da ’yanci mu yi ta yawo;
ba za mu ƙara zuwa wurinka ba’?
32 Budurwa za tă manta da kayan adonta
amarya ta manta da kayan adon aurenta?
Duk da haka mutanena sun manta da ni,
kwanaki ba iyaka.
33 Kuna da azanci sosai a bin masoya!
Kai, ko mafiya muni cikin mata tana iya koya daga hanyoyinku.
34 A rigunanku mutane kan sami
jinin matalauta marasa laifi,
ko da yake ba ku kama su suna fasawa su shiga ba.
Duk da haka
35 kuna cewa, ‘Ba ni da laifi;
ba ya fushi da ni.’
Amma zan zartar da hukunci a kanku
domin kun ce, ‘Ban yi zunubi ba.’
36 Don me kuke yawo da yawa haka,
kuna ta canjin hanyoyinku?
Masar za tă kunyata ku

yadda kuka sha kunya a wurin Assuriya.
37 Za ku kuma bar wurin
da hannuwanku a kanku,
gama UBANGIJI ya ƙi waɗanda kuka amince da su;
ba za ku zama abin taimako a gare su ba.

# 3

1 “In mutum ya saki matarsa
ta kuwa bar shi ta auri wani mutum,
zai iya komo da ita kuma?
Kasar ba za tă ƙazantu gaba ɗaya ba?
Amma kun yi rayuwa kamar karuwa da masoya masu yawa
yanzu za ki komo wurina?”
In ji UBANGIJI.
2 “Ta da idanu ki duba tsaunuka ki gani.
Akwai wani wurin da ba a kwana da ke ba?
A gefen hanya kin zauna kina jiran masoyanki,
kin zauna kamar makiyayi* a hamada.
Kin ƙazantar da ƙasar
da karuwancinki da muguntarki.
3 Saboda haka an hana yayyafi,
kuma babu ruwan bazara da ya sauka.
Duk da haka kina da irin kallon da karuwa takan yi;
kin ƙi ki ji kunya.
4 Yanzu ba kin kira ni,
‘Mahaifina, abokina daga ƙuruciyata ba,
5 kullum za ka riƙa fushi?
Hasalarka za tă ci gaba har abada ne?’
Haka kike magana,
amma kina aikata dukan muguntar da kika iya yi.”

### *Isra’ila marar aminci*

6 A zamanin Sarki Yosiya, UBANGIJI ya ce mini, “Ka ga abin da marar amincin nan,
Isra’ila ta yi? Ta haura kan kowane tudu mai tsayi da kowane gindin itace mai
duhuwa ta yi zina a can. 7 Na yi zaton bayan ta yi wannan duka, za tă komo wurina
amma ba tă yi haka ba, ’yar’uwarta marar aminci nan Yahuda ta gani. 8 Na ba wa
Isra’ila marar bangaskiya takardar saki na kuwa kore ta saboda duk zinanta. Duk da
haka na ga cewa ’yar’uwarta marar amincin nan Yahuda ba ta da tsoro; ita ma ta fita
ta yi zina. 9 Domin fasikancin Isra’ila bai yi tasiri gare ta ba, sai ta ƙazantar da ƙasar
ta kuma yi zina da dutse da kuma itace. 10 Duk da wannan duka, Yahuda ’yar’uwarta
rashin amincin ba tă komo gare ni da dukan zuciyarta ba, sai a munafunce,” in ji
UBANGIJI.
11 UBANGIJI ya ce mini, “Isra’ila marar bangaskiya ta fi Yahuda marar aminci. 12 Ka
tafi, ka yi shelar saƙon nan wajen arewa cewa,
“ ‘Ki komo, Isra’ila marar bangaskiya,’ in ji UBANGIJI,
‘Ba zan ƙara yin fushi da ke ba,
gama ni mai jinƙai ne,’ in ji UBANGIJI,
‘Ba zan yi fushi da ke har abada ba.
13 Ki dai yarda da laifinki

* 3:2 Ko kuwa mutumin Arab

kin yi wa UBANGIJI Allahnki tawaye,
kin watsar da alheranki ga baƙin alloli
a ƙarƙashin kowane itace mai duhuwa,
ba ki kuwa yi mini biyayya ba,' "
in ji UBANGIJI.

14 "Ku komo, ku mutane marasa bangaskiya," in ji UBANGIJI, "gama ni ne mijinku.
Zan ɗauke ku, ɗaya daga garuruwanku da kuma biyu daga zuriyarku in kawo ku
a Sihiyona. 15 Sa'an nan zan ba ku makiyaya da suke yin abin da zuciyata take so,
waɗanda za su bishe ku da sani da kuma fahimi. 16 A kwanakin, sa'ad da kuka ƙaru
sosai a ƙasar," in ji UBANGIJI, "mutane ba za su ƙara yin magana a kan, 'Akwatin
alkawarin UBANGIJI ba.' Ba zai ƙara shiga zuciyarsu ko su tuna ba; ko su bukace shi,
ko kuwa su yi wani irinsa ba. 17 A lokacin za su ce da Urushalima Kursiyin UBANGIJI,
kuma dukan al'ummai za su taru a Urushalima don su girmama sunan UBANGIJI. Ba
za su ƙara bin taurinkai zuciyarsu mai mugunta ba. 18 A kwanakin gidan Yahuda
zai haɗu da gidan Isra'ila, tare kuma za su zo daga ƙasar da take wajen arewa zuwa
ƙasar da na ba kakanninsu gādo.

19 "Ni kaina na faɗa,
" 'Da farin ciki zan ɗauke ki kamar 'ya'yana maza
in ba ki ƙasa mai daɗi,
gādo mafi kyau da wata al'umma.'
Na zaci za ki kira ni 'Mahaifi'
ba za ki ƙara rabuwa da bina ba.
20 Amma kamar mace marar aminci ga mijinta,
haka kika kasance marar aminci gare ni, ya gidan Isra'ila,"
in ji UBANGIJI.

21 An ji kuka a filayen tuddai,
kuka da roƙon mutanen Isra'ila,
domin sun lalace hanyoyinsu
sun kuma manta da UBANGIJI Allahnsu.

22 "Ku komo, mutane marasa bangaskiya;
zan warkar da ku daga ja da bayanku."

"I, za mu zo wurinka,
gama kai ne UBANGIJI Allahnmu.
23 Tabbatacce hayaniyar bin gumaka a kan tuddai
da duwatsu banza ne;
tabbatacce a wurin UBANGIJI Allahnmu ne
akwai ceton Isra'ila.
24 Daga ƙuruciyarmu allolin kunya sun cinye mu
amfanin wahalar kakanninmu
garkunan tumakinsu da na awakinsu,
yaransu maza da mata.
25 Bari mu kwanta mu sha kunya,
bari kuma kunyarmu ta rufe mu.
Mun yi wa UBANGIJI Allahnmu zunubi,
da mu da kakanninmu;
daga ƙuruciyarmu har yă zuwa yau
ba mu yi wa UBANGIJI Allahnmu biyayya ba."

# 4

1 “In za ka komo, ya Isra’ila,
ka komo gare ni,”
in ji UBANGIJI.
“In ka kau da gumakanka masu banƙyama daga gabana
ba ka ƙara karkace ba,
2 kuma in cikin gaskiya da adalci
ka rantse, ‘Muddin UBANGIJI yana raye,’
to al’ummai za su sami albarka ta wurinsa
kuma a cikinsa za su ɗaukaka.”
3 Ga abin da UBANGIJI yana ce wa mutanen Yahuda da kuma na Urushalima.
“Ku nome ƙasarku
kuma kada ku yi shuka cikin ƙayayyuwa.
4 Ku yi wa kanku kaciya ga UBANGIJI
ku yi wa zukatanku kaciya,
ku mutanen Yahuda da mutanen Urushalima,
in ba haka ba hasalata za tă sauko ta ci kamar wuta
saboda muguntar da kuka aikata
za tă ci ba wanda zai kashe ta.

*Masifa daga Arewa*

5 “Ku yi shela a Yahuda ku kuma furta a Urushalima ku ce,
‘Ku busa ƙaho a ko’ina a ƙasar!’
Ku tā da murya da ƙarfi ku ce,
‘Ku tattaru!
Bari mu gudu zuwa birane masu katanga!’
6 Ku tā da tuta don zuwa Sihiyona!
Ku gudu ku nemi mafaka ba tare da jinkiri ba!
Gama ina kawowa masifa daga arewa,
mummunan hallaka kuwa.”

7 Zaki ya fito daga ruƙuƙinsa;
mai hallakarwar al’ummai ya kama hanya.
Ya bar wurinsa
don yă lalace ƙasarku.
Garuruwanku za su zama kufai
babu mazauna.
8 Saboda haka ku yafa tufafin makoki,
ku yi makoki da kuka,
gama fushin UBANGIJI
bai juye daga gare mu ba.

9 “A wannan rana,” in ji UBANGIJI,
“sarki da shugabanni za su fid da zuciya,
firistoci za su razana,
annabawa kuma za su yi mamaki.”
10 Sai na ce, “Kash, UBANGIJI Mai Iko Duka, yaya ka ruɗi mutanen nan da kuma
Urushalima gaba ɗaya haka ta wurin cewa, ‘Za ku zauna lafiya,’ sa’ad da takobi
yana a maƙogwaronmu.”
11 A lokacin za a faɗa wa mutanen nan da kuma Urushalima cewa, “Iska mai zafi
daga tuddan hamada za tă hura zuwa wajen mutanena, amma ba don ta sheƙe ko

ta rairaye; ba; 12 iska mafificin ƙarfi da ta fito daga gare ni.* Yanzu na zartar da hukuncina a kansu.”
13 Duba! Yana zuwa kamar gizagizai,
kekunan yaƙinsa suna zuwa kamar guguwa,
dawakansa sun fi gaggafa sauri.
Kaiton mu! Mun shiga uku!
14 Ya Urushalima, ki wanke mugunta daga zuciyarki ki sami ceto.
Har yaushe za ki zauna riƙe da mugayen tunani?
15 Murya ta shela daga Dan,
tana furtawa masifa daga tuddan Efraim.
16 “A faɗa wa al’ummai wannan,
a furta wannan game Urushalima.
‘Sojoji masu ƙawanya suna zuwa daga ƙasa mai nisa,
suna tā da kirarin yaƙi a kan biranen Yahuda.
17 Sun kewaye ta kamar masu gadin fili,
domin ta yi mini tawaye,’ ”
in ji UBANGIJI.
18 “Halinki da ayyukanki
sun kawo wannan a kanki.
Hukuncinki ke nan.
Yana da ɗaci!
Ya soke ki har zuciyarki!”

19 Azabana, azabana!
Ina birgima cikin zafi.
Azabana, azabar zuciyata!
Zuciyata yana bugu a cikina,
Ba zan yi shiru ba.
Gama na ji karan ƙaho;
na ji kirarin yaƙi.
20 Masifa kan masifa;
dukan ƙasar ta zama kufai.
Cikin ɗan lokaci aka rurrushe tentuna nawa,
mafakata ba zato.
21 Har yaushe zan dubi tutar yaƙi
in kuma ji karar ƙaho?

22 “Mutanena wawaye ne;
ba su san ni ba.
Su ’ya’ya ne marasa azanci;
ba su da fahimi.
Suna da dabarar aikata mugunta;
ba su san yadda za su aikata alheri ba.”

23 Na dubi duniya,
na ga cewa marar siffa ce babu kome;
sammai kuma,
haskensu ya tafi.
24 Na dubi duwatsu,
sai na ga suna makyarkyata;
dukan tuddai kuwa suna lilo.

* 4:12 Ko kuwa ta zo ta wurin umarnina

25 Na duba, sai na ga ba kowa;
kowane tsuntsu a sarari da ya tsere.
26 Na duba, sai na ga ƙasa mai amfani ta zama hamada;
dukan garuruwanta sun zama kufai
a gaban UBANGIJI, a gaban zafin fushinsa.
27 Ga abin da UBANGIJI yana cewa,
"Dukan ƙasar za tă zama kufai,
ko da yake ba zan hallaka ta gaba ɗaya ba.
28 Saboda haka duniya za tă yi kuka
sammai a bisa kuma za su yi duhu,
domin na yi magana kuma ba zan fasa ba,
na yanke shawara ba kuwa zan janye ba."

29 Da jin motsin mahayan dawakai da maharba
kowane gari ya ruga da gudu.
Waɗansu suka shiga kurmi;
waɗansu suka hau cikin duwatsu.
Dukan garuruwan sun fashe tas;
babu wani da yake zama a ciki.

30 Me kike yi, ya wadda aka ragargaza?
Me ya sa kika sanya mulufi
kika sa kayan adon zinariya?
Me ya sa kika sa wa idanunki tozali?
Kin yi kwalliyarki a banza.
Masoyanki sun bar ki;
suna neman ranki.

31 Na ji kuka kamar na mace mai naƙuda,
nishi kamar na wadda take haihuwa ɗanta na fari,
kukan Diyar Sihiyona tana haki, da ƙyar take numfashi,
tana miƙa hannuwanta tana cewa,
"Wayyo ni kaina! Na suma;
an ba da raina ga masu kisana."

# 5

*Ba ko ɗaya da yake da adalci*

1 "Ku yi ta kai da kawowa a titunan Urushalima,
ku dudduba ko'ina ku kuma lura,
ku bincika cikin dandalinta.
Ko za ku sami mutum guda
wanda yake aikata adalci wanda yake kuma son bin gaskiya,
sai in gafarta wa wannan birni.
2 Ko da yake suna cewa, 'Muddin UBANGIJI yana raye,'
duk da haka suna rantsuwar ƙarya."

3 Ya UBANGIJI, idanunka ba sa ganin gaskiya?
Ka buge su, amma ba su ji zafi ba;
ka ragargaza su, amma suka ƙi su gyara.
Fuskarsu ta ƙeƙashe fiye da dutse
suka ƙi su tuba.

4 Na yi tunani, “Waɗannan ne kawai matalauta;
su wawaye ne,
gama ba su san hanyar UBANGIJI ba,
ko abubuwan da Allahnsu yake bukata ba.
5 Saboda haka zan tafi wurin shugabanni
in yi musu magana;
tabbatacce sun san hanyar UBANGIJI,
da abubuwan da Allahnsu yake bukata.”
Amma da nufi guda su ma suka karye karkiyar
suka tsintsinke sarƙoƙin.
6 Saboda haka zaki daga kurmi zai fāɗa musu,
kyarkeci kuma daga hamada zai cinye su,
damisa za tă yi musu ƙawanya kusa da garuruwansu
yă yayyage duk wanda ya kuskura ya fita,
gama tawayensu da girma yake
jan bayansu kuma yana da yawa.

7 “Me zai sa in gafarta muku?
’Ya’yanku sun yashe ni
sun yi rantsuwa da allolin da ba alloli ba ne.
Na biya musu dukan bukatunsu,
duk da haka suka yi zina
suka tattaru a gidajen karuwai.
8 An ciyar da su sosai, kamar ƙosassun ingarmu,
masu jaraba,
kowanne yana haniniya, yana neman matar maƙwabcinsa.
9 Ba zan hukunta su saboda wannan ba?” In ji UBANGIJI.
“Bai kamata in yi ramuwa
a kan irin al’ummar nan ba?

10 “Ku ratsa cikin gonakin inabinta ku cinye su,
amma kada ku hallaka su gaba ɗaya.
Ku kakkaɓe rassanta,
gama waɗannan mutane ba na UBANGIJI ba ne.
11 Gidan Isra’ila da gidan Yahuda
sun zama marasa aminci gaba ɗaya gare ni”
in ji UBANGIJI.

12 Sun yi ƙarya a kan UBANGIJI;
sun ce, “Ba zai yi kome ba!
Ba wata masifar da za tă same mu;
ba za mu taɓa ganin takobi ko yunwa ba.
13 Annabawa holoƙo ne kawai
maganar kuwa ba ta cikinsu;
saboda haka bari abin da suke faɗi ya koma kansu.”
14 Saboda haka ga abin UBANGIJI Allah Maɗaukaki yana cewa,
“Domin mutanen sun yi waɗannan maganganu,
zan mai da maganata a bakinku wuta
waɗannan mutane kuwa su zama itacen da za tă ci.
15 Ya gidan Isra’ila,” in ji UBANGIJI,
“Ina kawo al’umma daga nesa a kanku

al'umma ce ta tun dā mai ƙarfin hali,
mutane ne da ba ku san harshensu ba,
waɗanda ba za ku fahimci abin da suke faɗa ba.
16 Kwarinsu kamar buɗaɗɗen kabari ne;
dukansu jarumawa ne.
17 Za su cinye amfanin gonakinku da abincinku,
za su cinye 'ya'yanku maza da mata;
za su cinye garkunan tumakinku da na awakinku,
za su cinye 'ya'yan inabinku da na ɓaurenku.
Da takobi za su hallaka
biranenku masu katanga.

18 "Amma ko a cikin waɗancan kwanaki," in ji UBANGIJI, "ba zan hallaka ku gaba
ɗaya ba. 19 Sa'ad da kuma mutanen suka yi tambaya, 'Me ya sa UBANGIJI Allahnmu
ya yi dukan wannan gare mu?' Sai ka amsa musu, 'Yadda kuka yashe ni kuka kuma
bauta wa baƙin alloli a ƙasarku, haka yanzu za ku bauta wa baƙi a ƙasar da ba taku
ba.'

20 "Ka sanar da wannan ga gidan Yaƙub
ka yi shelarsa a Yahuda.
21 Ku ji wannan, ku wawaye marasa azanci,
waɗanda suke da idanu amma ba sa gani,
waɗanda suke da kunnuwa amma ba sa ji.
22 Bai kamata ku ji tsorona ba?" In ji UBANGIJI.
"Bai kamata ku yi rawar jiki a gabana ba?
Na sa yashi ya zama iyakar teku,
madawwamiyar iyakar da ba zai tsallake ba.
Raƙuman ruwa za su iya yin hauka, amma ba za su iya haye ta ba;
za su iya yin ruri, amma ba za su iya ƙetare ta ba.
23 Amma mutanen nan suna da tauraren zukata, kuma 'yan tawaye ne;
sun kauce suka kuma rabu da ni.
24 Ba sa faɗa wa kansu, 'Bari mu ji tsoron UBANGIJI Allahnmu,
wanda yake ba mu ruwan sama a kan kari na kaka da na bazara,
wanda kullum yake tabbatar mana da girbi.'
25 Laifofinku sun raba ku da waɗannan abubuwa;
zunubanku sun hana ku samun alheri.

26 "A cikin mutanena an sami mugaye
waɗanda suke kwanton ɓauna kamar masu sa tarko wa tsuntsaye
kamar waɗanda suke kafa tarko don su kama mutane.
27 Kamar keji cike da tsuntsaye,
gidajensu sun cika da ruɗu;
sun yi arziki suka kuma zama masu iko
28 suka kuma yi ƙiba, suka yi bul-bul.
Mugayen ayyukansu ba su da iyaka;
ba sa wa marayu shari'ar adalci,
ba sa kāre 'yancin matalauta.
29 Bai kamata in hukunta su saboda wannan ba?"
In ji UBANGIJI.
"Bai kamata in yi ramuwa
a kan irin al'umma kamar wannan ba?

30 "Abin banmamaki da bantsoro
ya faru a ƙasar.

31 Annabawa suna annabcin ƙarya,
firistoci suna mulki da ikon kansu,
mutanena kuma suna son haka.
Amma me za ku yi a ƙarshe?

# 6

*Abokan gāba sun kewaye Urushalima*

1 "Ku gudu neman mafaka, mutanen Benyamin!
Ku gudu daga Urushalima!
Ku busa ƙaho a Tekowa!
Ku ba da alama a Bet-Hakkerem!
Gama masifa tana zuwa daga arewa,
mummunar hallaka ce kuwa.
2 Zan hallaka Diyar Sihiyona,
kyakkyawa da kuma mai laulayi.
3 Makiyaya da garkunansu za su taso mata;
za su kafa tentunansu kewaye da ita,
kowanne yana lura da sashensa."

4 "Mu shirya don yaƙi da ita!
Ku tashi, bari mu fāɗa mata da tsakar rana!
Amma, kaito, rana tana fāɗuwa,
inuwar yamma kuwa sai ƙaran tsawo take.
5 Saboda haka ku tashi, bari mu fāɗa mata da dare
mu rurrushe kagaranta!"
6 Ga abin da UBANGIJI Maɗaukaki yana cewa,
"Ku sassare itatuwan
ku tula ƙasa kewaye da Urushalima.
Dole a hukunta wannan birni;
saboda ya cika da zalunci.
7 Kamar yadda rijiya takan ba da ruwarta,
haka birnin yake da muguntarsa.
Ana jin labarin rikici da hallaka a cikinsa;
ciwonsa da mikinsa kullum suna a gabana.
8 Ki ji gargaɗi, ya Urushalima,
ko kuwa in juya daga gare ki
in mai da ƙasarki kufai
don kada wani ya zauna a cikinta."
9 Ga abin da UBANGIJI Maɗaukaki yana cewa,
"Bari su yi kalan raguwar Isra'ila
a yi kalan sarai yadda ake yi wa inabi;
ka sāke miƙa hannunka a kan rassan,
kamar mai tattara inabi."

10 Ga wa zan yi magana in kuma gargaɗar?
Wa zai saurare ni?
Kunnuwansu sun toshe*
don kada su ji.
Maganar UBANGIJI ta zama abin zargi a gare su;
ba sa jin daɗinta.
11 Amma ina cike da fushin UBANGIJI,

* **6:10** Da Ibraniyanci marar kaciya

kuma ba na iya kannewa.

"Ka kwararo shi a kan yara a titi
da kuma a kan samarin da suka tattaru;
za a kama miji da mata a cikinsa,
tsofaffi da suka tsufa tukub.
12 Za a ba da gidajensu ga waɗansu,
tare da gonakinsu da matansu,
sa'ad da na miƙa hannuna
gāba da waɗanda suke zama a ƙasar,"
in ji UBANGIJI.
13 "Daga ƙarami zuwa babba,
dukansu masu haɗama ne don riba;
har da annabawa da firistoci,
dukansu suna aikata rashin gaskiya.
14 Sukan ɗaura mikin mutanena
sai ka ce mikin ba shi da matsala.
Suna cewa, 'Lafiya, Lafiya,'
alhali kuwa ba lafiya.
15 Suna jin kunyar halinsu na banƙyama?
A'a, ba sa jin kunya sam;
ba su ma san yadda za su soke kai ba.
Saboda haka za su fāɗi tare da fāɗaɗɗu;
za a hamɓarar da su sa'ad da na hukunta su,"
in ji UBANGIJI.
16 Ga abin da UBANGIJI yana cewa,
"Ku tsaya kan hanyoyi, ku duba;
ku nemi hanyoyin dā,
ku tambaya inda hanyar mai kyau take, ku yi tafiya a kanta,
za ku kuwa sami hutu wa rayukanku.
Amma kun ce, 'Ba za mu bi ta ba.'
17 Na naɗa muku masu tsaro a kanku na kuma ce,
'Ku saurari karan ƙaho!'
Amma kuka ce, 'Ba za mu saurara ba.'
18 Saboda haka ku, ya al'ummai;
ku lura Ya shaidu,
abin da zai faru da su.
19 Ki ji, ya duniya.
Zan kawo masifa a kan waɗannan mutane,
sakayyar ƙulle-ƙullensu,
domin ba su saurari maganata ba
suka kuma ƙi dokata.
20 Babu riba a kawo mini turare daga Sheba
ko rake mai zaƙi daga ƙasa mai nisa?
Ba zan karɓi hadayunku na ƙonawa ba;
ba na jin daɗin sadakokinku."
21 Saboda haka ga abin da UBANGIJI yana cewa,
"Zan sa abin tuntuɓe gaban mutanena.
Mahaifi da 'ya'yansa maza za su yi tuntuɓe a kan juna;
maƙwabci da abokansa za su hallaka."
22 Ga abin da UBANGIJI yana cewa,
"Duba, sojoji suna zuwa

daga ƙasar arewa;
babbar al'umma ce ta yunƙuro
daga iyakokin duniya.
23 Suna riƙe da baka da māshi;
mugaye ne kuma marasa tausayi.
Motsinsu kamar ƙugin teku ne
yayinda suke hawan dawakansu;
suna zuwa a jere kamar wanda ya yi shirin yaƙi
don su fāɗa miki, ya Diyar Sihiyona."

24 Mun ji labari a kansu,
hannuwanmu kuwa suka yi laƙwas.
Azaba ta kama mu,
zafi kamar na mace mai naƙuda.
25 Kada ku fita zuwa gonaki
ko ku yi tafiya a hanyoyi,
gama abokin gāba yana da takobi,
kuma akwai razana ko'ina.
26 Ya mutanena, ku sanya tufafin makoki
ku yi birgima a toka;
ku yi kuka mai zafi
irin wanda akan yi wa ɗa tilo,
gama nan da nan mai hallakarwa
zai auko mana.

27 "Na maishe ka mai jarrabawar ƙarfe
mutanena ne kuwa ƙarfen,
don ka lura
ka kuma gwada hanyoyinsu.
28 Su duka masu taurinkai ne, 'yan tawaye,
suna yawo suna baza jita-jita.
Su tagulla ne da ƙarfe;
dukansu lalatattu ne.
29 Mazuga yana zuga da ƙarfi
don yă ƙone dalma da wuta,
amma tacewa yana tafiya a banza;
ba a fitar da mugaye.
30 Ana ce da su azurfar da aka ƙi,
gama UBANGIJI ya ƙi su."

# 7

*Banzancin addinin ƙarya*
*(Irmiya 26.1-6)*

1 Maganar da ta zo wa Irmiya ke nan daga UBANGIJI. 2 "Ka tsaya a ƙofar gidan
UBANGIJI, a can kuwa ka yi shelar wannan saƙo.
" 'Ku ji maganar UBANGIJI, dukanku mutanen Yahuda waɗanda suke shiga ta
waɗannan ƙofofi don yin sujada ga UBANGIJI. 3 Ga abin da UBANGIJI Maɗaukaki,
Allahna Isra'ila, yana cewa ku gyara hanyoyinku da ayyukanku, zan kuwa bar ku
ku zauna a wannan wuri. 4 Kada ku dogara ga maganganun nan na ruɗarwa cewa,
"Wannan shi ne haikalin UBANGIJI, haikalin UBANGIJI, haikalin UBANGIJI!" 5 In dai
kuka canja hanyoyinku da ayyukanku kuma kuna aikata adalci da junanku, 6 in ba

ku zalunci baƙo, maraya ko gwauruwa ba kuma in ba ku zub da jinin marar laifi
a wannan wuri ba, in kuma ba ku bi waɗansu alloli da za su cuce ku ba, 7 to, zan
bar ku ku zauna a wannan wuri, a ƙasar da na ba kakanninku har abada abadin.
8 Amma ga shi, kuna dogara ga maganganu na ruɗami marasa amfani.
9 " 'Za ku yi sata da kisa, ku yi zina da rantsuwar ƙarya, kuna ƙone turare wa Ba'al
kuna kuma bin waɗansu allolin da ba ku sani ba, 10 sa'an nan ku zo ku tsaya a gabana
a wannan gida, wanda ake kira da Sunana, kuna cewa, "An cece mu," mun dace mu
aikata waɗannan abubuwa banƙyama? 11 Wannan gidan da ake kira da Sunana ya
zama kogon 'yan fashi ne a gare ku? Amma ina kallo! In ji UBANGIJI.
12 " 'Yanzu ku fita zuwa Shilo inda na fara maishe shi wurin zama don Sunana, ku
ga abin da na yi masa saboda muguntar mutanen Isra'ila. 13 Yayinda kuke yin dukan
waɗannan abubuwa, in ji UBANGIJI, na yi muku magana sau da sau, amma ba ku ji
ba; na kira ku, amma ba ku amsa ba. 14 Saboda haka, abin da na yi wa Shilo shi ne
yanzu zan yi wa gidan da ake kira da Sunana, haikalin da kuka dogara a kai, wurin
da na ba ku da kuma kakanninku. 15 Zan kore ku daga gabana, kamar yadda na yi
ga dukan 'yan'uwanku, mutanen Efraim.'
16 "Saboda haka kada ka yi addu'a don wannan mutane ko ka yi wani kuka ko roƙo
dominsu, gama ba zan ji ka ba. 17 Ba ka gani abin da suke yi a biranen Yahuda da
kuma a titunan Urushalima? 18 Yara sukan tara itace, iyaye suka hura wuta, mata
kuma sukan kwaɓa kullu don su yi wa Sarauniyar Sama waina. Sukan miƙa hadayun
sha ga waɗansu alloli don su tsokane ni in yi fushi. 19 Amma ni ne suke tsokana? In
ji UBANGIJI Ashe, ba kansu ne suke cuta, suna kunyata kansu ba?
20 " 'Saboda haka ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa fushina da hasalata
za su kwarara a wannan wuri, a kan mutum da dabba, a kan itatuwan fili da a kan
amfanin gona, za su yi ta kuna, ba kuwa za a kashe ba.
21 " 'Ga abin da UBANGIJI Maɗaukaki, Allah na Isra'ila yana cewa ci gaba, ku ƙara
hadayun ƙonawarku da sauran sadakoki ku kuma yi ta cin naman! 22 Gama sa'ad da
na fitar da kakanninku daga Masar na kuma yi musu magana, ban ba su dokoki kawai
game da hadayun ƙonawa da sadakoki ba, 23 amma na ba su wannan umarni cewa ku
yi mini biyayya, zan kuwa zama Allahnku ku kuma ku zama mutanena. Ku yi tafiya
cikin dukan hanyoyin da na umarce ku, don ku zauna lafiya. 24 Amma ba su saurara
ba, ba su kuwa kula ba; a maimako, suka bi shawarar kansu da ta taurare muguwar
zukatansu. Su ja da baya a maimakon yin gaba. 25 Daga lokacin da kakanninku suka
bar Masar har yă zuwa yau, kullum na yi ta aikan bayina annabawa. 26 Amma ba su
saurare ni ba, ba su kula ba. Sai suka taurare zukatansu suka aikata mugun abu fiye
da na kakanninsu.'
27 "Sa'ad da ka faɗa musu wannan duka, ba za su saurare ka ba; sa'ad da ka kira
su, ba za su amsa ba. 28 Saboda haka ka faɗa musu cewa, 'Wannan ce al'ummar da
ba tă yi biyayya ga UBANGIJI Allahnta ba, ba kuwa ta karɓi gyara ba. Gaskiya ta ƙare;
ta ɓace gaba ɗaya daga leɓunansu.
29 " 'Ku aske gashin kanku ku zubar; ku yi makoki a filayen tuddai, gama UBANGIJI
ya ƙi 'yan zamanin nan ya kuma rabu da su saboda fushin da suka ba shi.

### *Kwarin kisa*

30 " 'Mutanen Yahuda sun yi mugunta a gabana, in ji UBANGIJI. Sun kafa gumakansu
masu banƙyama a gidan da ake kira da Sunana suka ƙazantar da shi. 31 Sun gida
masujadan Tofet a Kwarin Ben Hinnom don miƙa 'ya'yansu maza da mata a wuta,
abin da ban yi umarni ba, ba kuwa yi tunaninsa ba. 32 Saboda haka ku yi hankali,
kwanaki suna zuwa in ji UBANGIJI, sa'ad da mutane ba za su ƙara kira wurin Tofet
ko Kwarin Ben Hinnom ba, amma Kwarin Kisa, gama za su binne matattu a Tofet sai
har ba sauran wuri. 33 Sa'an nan gawawwakin wannan mutane za su zama abinci

ga tsuntsayen sama da kuma namun jeji, ba za a kuwa sami wani da zai kore su
ba. 34 Zan kawo ƙarshen muryar murna da farin ciki da muryar amarya da ango a
garuruwan Yahuda da kuma a titunan Urushalima, gama ƙasar za tă zama kufai.

# 8

1 " 'A wancan lokaci, in ji UBANGIJI, za a fitar da ƙasusuwan sarakuna da na
shugabannin Yahuda, ƙasusuwan firistoci da na annabawa, da kuma ƙasusuwan
mutanen Urushalima daga kaburbura. 2 Za a shimfiɗa su a rana da wata da kuma
dukan taurarin sammai, waɗanda suka ƙaunata suka kuma bauta wa, waɗanda suka
bi suka nemi shawarar suka kuma yi wa sujada. Ba za a tattara su ko a binne su ba,
amma za su zama kamar juji a jibge a ƙasa. 3 Duk inda na kore su zuwa, dukan
waɗanda suka ragu na wannan muguwar al'umma za su gwammaci mutuwa da rai,
in ji UBANGIJI Maɗaukaki.'

4 "Fada musu cewa, 'Ga abin da UBANGIJI yana cewa,
" 'Sa'ad da mutane suka fāɗi, ba sa tashi ne?
Sa'ad da mutum ya kauce, ba ya dawowa?
5 To, me ya sa waɗannan mutane suka kauce?
Me ya sa Urushalima kullum take kaucewa?
Sun manne wa ƙarya;
suka ƙi su dawo.
6 Na saurara sosai,
amma ba su faɗi wata maganar kirki ba.
Ba wanda ya tuba daga muguntarsa,
sai ma cewa yake, "Me na yi?"
Kowa ta kai-ta-kai yake
kamar dokin da ya kutsa kai a fagen fama.
7 Ko shamuwa ta sararin sama ma
takan san lokutan da aka tsara mata,
kurciya, mashirare da kuma zalɓe
sukan lura da lokacin ƙauransu.
Amma mutanena ba su san
abubuwan da UBANGIJI yake bukata ba.

8 " 'Yaya za ku ce, "Muna da hikima,
gama muna da dokar UBANGIJI,"
alhali alƙalamin ƙarya na magatakarda
ya yi ƙarya?
9 Za a kunyatar da masu hikima;
za su yi fargaba a kuma kama su.
Da yake sun ƙi maganar UBANGIJI,
wace irin hikima kuka ce kuke da ita?
10 Saboda haka zan ba da matansu ga waɗansu
gonakinsu kuma ga waɗansu da suka ci da yaƙi.
Tun daga ƙarami har zuwa babba,
kowannensu yana haɗamar cin muguwar riba;
har da annabawa da firistoci ma,
kowannensu yana ƙarya.
11 Sukan ɗaura mikin mutanena
sai ka ce mikin ba shi da matsala.
Suna cewa, "Lafiya, Lafiya,"
alhali kuwa ba lafiya.
12 Sukan ji kunyar halin banƙyamarsu kuwa?

Sam, ba su da kunya ko kaɗan;
ba su ma san yadda za su ji kunya ba.
Saboda haka sukan fāɗi tare da fāɗaɗɗu;
za su fāɗi sa'ad da aka hukunta su,
in ji UBANGIJI.

13 " 'Zan ƙwace girbinsu,
in ji UBANGIJI.
Ba a za sami inabi a kuringa ba.
Ba za a sami 'ya'ya a itacen ɓaure ba,
ganyayensu kuwa za su bushe.
Abin da na ba su
za a ƙwace.' "

14 Me ya sa muke zama a nan?
Mu tattaru!
Mu gudu zuwa birane masu katanga
mu mutu a can!
Gama UBANGIJI Allahnmu ya ƙaddara mana mutuwa
ya kuma ba mu ruwan dafi mu sha,
domin mun yi masa zunubi.
15 Mun sa zuciya ga salama
amma ba lafiya,
mun sa zuciya ga lokacin warkarwa
amma sai ga razana.
16 Daga Dan ana jin
tirjin dawakan abokin gāba;
da jin haniniyar ingarmunsu
dukan ƙasar ta girgiza.
Sun zo su cinye
ƙasar da kome da yake cikinta,
birni da dukan mazaunanta.

17 "Duba, zan aika macizai masu dafi a cikinku,
kāsā, waɗanda ba su da maƙari,
za su kuwa sassare ku,"
in ji UBANGIJI.

18 Ya mai ta'aziyyata a cikin baƙin ciki,
zuciyata ta ɓaci ƙwarai.
19 Ka saurari kukan mutanena
daga ƙasa mai nisa suna cewa,
"UBANGIJI ba ya a Sihiyona ne?
Sarkinta ba ya can ne kuma?"

"Me ya sa suka tsokane ni da gumakansu har na yi fushi,
da baƙin gumakansu marasa amfani?"

20 "Girbi ya wuce,
damuna ta ƙare,
ba a kuwa cece mu ba."

21 Da yake an ragargazar da mutanena, an ragargaza ni ke nan;
na yi kuka, tsoro ya kama ni.
22 Ba magani ne a Gileyad?
Ba likita ne a can?
To, me ya sa ba warkarwa
wa raunin mutanena?

# 9

1 Da ma kaina maɓulɓulan ruwa ne
idanuna kuma maɓulɓulan hawaye!
Da sai in yi kuka dare da rana
saboda mutanena da aka kashe.
2 Da ma a hamada
ina da wurin da matafiye za su sauka,
don in bar mutanena
in tafi in bar su;
gama dukansu mazinata ne,
taron mutane marasa aminci.

3 "Sun tanƙwasa harshensu
kamar baka, don su harba ƙarya;
ba da gaskiya ba ne
suke nasara a cikin ƙasar.
Sukan tashi daga wannan zunubi zuwa wancan;
ba su san ni ba,"
in ji UBANGIJI.
4 "Ka yi hankali da abokanka;
kada ka amince da 'yan'uwanka.
Gama kowane ɗan'uwa munafuki ne,
kowane aboki kuma mai kushe ne.
5 Aboki kan ruɗi aboki,
ba mai faɗar gaskiya.
Sun koya wa harshensu faɗar ƙarya;
sun gajiyar da kansu da yin zunubi.
6 Kai* kana zama a tsakiyar ruɗu;
cikin ruɗunsu sun ƙi su san ni,"
in ji UBANGIJI.
7 Saboda haka ga abin da UBANGIJI Maɗaukaki yana cewa,
"Ga shi zan tace in kuma gwada su,
gama me kuwa zan yi
saboda zunubin mutanena?
8 Harshensu kibiya ce mai dafi;
yana magana da ruɗu.
Da bakinsa kowa yana maganar alheri da maƙwabcinsa,
amma a zuciyarsa ya sa masa tarko.
9 Bai kamata in hukunta su saboda wannan ba?"
In ji UBANGIJI.
"Bai kamata in ɗau fansa
a kan irin al'umma kamar wannan ba?"

10 Zan yi kuka in yi kururuwa saboda duwatsu
in kuma yi makoki game da wuraren kiwon hamada.

* **9:6** Wato, Irmiya (jam'i na mutum guda a Ibraniyanci)

Sun zama kango ba wanda yake bi cikinta,
ba a kuma jin kukan shanu.
Tsuntsaye sararin sama sun gudu
namun jeji ma duk sun watse.

11 "Zan mai da Urushalima tsibin kufai,
wurin zaman diloli;
zan kuma lalace garuruwan Yahuda
saboda haka ba wanda zai zauna a can."
12 Wane mutum ne yana da isashiyar hikimar fahimtar wannan? Wa UBANGIJI ya
umarta da zai iya yin bayani? Me ya sa aka lalace ƙasar ta zama kufai kamar hamada
da ba wanda zai iya ratsa ta?
13 UBANGIJI ya ce, "Domin sun bar dokata, wadda na sa a gabansu; ba su yi biyayya
da ni ko su bi dokata ba. 14 A maimako, sun bi taurin zuciyarsu; suka bi Ba'al, yadda
kakanninsu suka koya musu." 15 Saboda haka, ga abin da UBANGIJI Maɗaukaki, Allah
na Isra'ila yana cewa, "Ga shi zan sa wannan mutane su ci abinci mai ɗaci su kuma
sha ruwan dafi. 16 Zan watsar da su a cikin al'ummai da su da kakanninsu ba su sani
ba, zan kuma fafare su da takobi sai na hallaka su."
17 Ga abin da UBANGIJI Maɗaukaki yana cewa,
"Ku lura yanzu! Ku kira mata masu makoki su zo
ku aika wa gwanaye a cikinsu su zo.
18 Bari su zo da sauri
su yi kuka a kanmu
sai idanunmu sun cika da hawaye
giranmu kuma su jiƙe sharkaf.
19 An ji karar kuka daga Sihiyona cewa,
'Duba yadda muka lalace!
Duba irin babban kunyar da muka sha!
Dole mu bar ƙasar
domin gidajenmu sun lalace.' "

20 Yanzu, ya mata, ku ji maganar UBANGIJI;
ku buɗe kunnuwanku ga maganar bakina.
Ku koya wa 'yan matanku yadda za su yi kuka;
ku koya wa juna makoki.
21 Mutuwa ta haura ta tagoginmu
ta kuma shiga katangarmu;
ta karkashe 'ya'ya a tituna
ta kuma karkashe samari a dandali.
22 Ka ce, "Ga abin da UBANGIJI ya furta,
" 'Gawawwakin mutane za su fāɗi
kamar juji a fili,
kamar hatsin da aka yanka a bayan mai girbi,
da ba mai tara su.' "
23 Ga abin da UBANGIJI yana cewa,
"Kada mai hikima ya yi fariya da hikimarsa
ko mai ƙarfi ya yi fariya da ƙarfinsa
ko mai arziki ya yi fariya da arzikinsa,
24 amma bari shi wanda yake taƙama ya yi taƙama da wannan,
cewa ya fahimci ya kuma san ni,
cewa ni ne UBANGIJI, wanda yake yin alheri,
gaskiya da kuma adalci a duniya,

gama a waɗannan ne nake jin daɗi,"
in ji UBANGIJI.
25 "Kwanaki suna zuwa," in ji UBANGIJI, "sa'ad da zan hukunta dukan waɗanda
aka yi musu kaciya kawai a jiki, 26 Masar, Yahuda, Edom, Ammon, Mowab da dukan
waɗanda suke zaune a hamada a wurare masu nisa.† Gama dukan waɗannan
al'ummai marasa kaciya ne, har dukan gidan Isra'ila ma marasa kaciya ne a zuciya."

# 10

*Allah da kuma gumaka*

1 Ku ji abin da UBANGIJI yana ce muku, ya gidan Isra'ila. 2 Ga abin da UBANGIJI yana
cewa,

"Kada ku koyi hanyoyin al'ummai
ko ku razana game da alamun sararin sama,
ko da yake al'ummai sun razana saboda su.
3 Gama al'adun mutane banza ne;
sukan yanke itace daga kurmi,
sai mai sassaƙa yă sassaƙa shi da gizago.
4 Sukan yi masa ado da azurfa da kuma zinariya;
sukan ɗauki guduma su kafa shi da ƙusoshi,
don kada yă fāɗi.
5 Kamar dodon gona cikin gonar kabewa,
haka gumakansu ba sa iya magana;
dole a yi ta ɗaukansu
domin ba za su iya tafiya ba.
Kada ku ji tsoronsu;
ba za su iya yi wa wani lahani ba
ba sa iya yin wani abin kirki."

6 Babu wani kamar ka, ya UBANGIJI;
kai mai girma ne,
kuma sunanka yana da girma da kuma iko.
7 Wane ne ba zai girmama ka ba,
Ya Sarkin al'ummai?
Tsoronka wajibi ne.
A cikin dukan masu hikima na al'ummai
kuma cikin dukan mulkokinsu,
babu kamar ka.

8 Dukansu marasa azanci ne wawaye;
gumakan itacen banza ne suke koya musu.
9 An kawo ƙeraren azurfa daga Tarshish
zinariya kuma daga Ufaz.
Abin da gwani da maƙerin zinariya suka yi
sa'an nan aka yi masa ado da mulufi da shunayya
dukan aikin gwanaye.
10 Amma UBANGIJI shi ne Allah na gaskiya;
shi ne Allah mai rai, madawwamin sarki.
Sa'ad da ya yi fushi, ƙasa takan girgiza;
al'ummai ba sa iya jure da hasalarsa.

† **9:26** Ko kuwa hamada da kuma waɗanda suke hawan gashi kai ta goshinsu

11 “Ka faɗa musu wannan, ‘Waɗannan alloli, waɗanda ba su yi sammai da ƙasa
ba, za su hallaka daga duniya da kuma daga ƙarƙashin sammai.’ ”*
12 Amma Allah ya yi duniya ta wurin ikonsa;
ya kafa duniya ta wurin hikimarsa
ya shimfiɗa sammai ta wurin fahiminsa.
13 Sa’ad da ya yi tsawa, ruwaye a cikin sammai sukan yi ƙugi;
yakan sa gizagizai su taso daga iyakokin duniya.
Yakan aiki walƙiya da ruwan sama
ya fitar da iska daga gidajen ajiyarsa.

14 Kowa marar azanci ne, marar ilimi;
kowane maƙerin zinariya zai sha kunya saboda gumakansa.
Siffofinsa ƙarya ne;
ba su da numfashi a cikinsu.
15 Su ba kome ba ne, aikin ruɗami ne;
Sa’ad da hukuncinsu ya yi za su lalace.
16 Shi da yake Rabon Yaƙub ba kamar waɗannan yake ba,
gama shi ne Mahaliccin abubuwa duka,
har da Isra’ila, kabilar gādonsa
Ubangiji Maɗaukaki ne sunansa.

### *Hallaka mai zuwa*

17 Ku tattara kayayyakinku don ku bar ƙasar,
ku da kuke zaune a wurin da aka kewaye da yaƙi.
18 Gama haka Ubangiji ya faɗa,
“A wannan lokaci zan jefar
da waɗanda suke zaune a ƙasar;
zan kawo damuwa a kansu
domin a kama su.”

19 Tawa ta ƙare, saboda raunin da aka yi mini!
Raunina ba mai warkewa ba ne!
Duk da haka na ce wa kaina,
“Wannan ciwona ne, dole kuma in jure da shi.”
20 An lalatar da tentina;
dukan igiyoyinsa sun tsintsinke.
’Ya’yana maza sun bar ni ba sa nan;
ba wanda aka bari da zai kafa tentina
ko ya kafa mini mafaka.
21 Makiyaya marasa azanci ne
kuma ba sa neman nufin Ubangiji;
saboda haka ba sa nasara
dukan garkensu kuwa ya watse.
22 Ku saurara! Rahoto yana zuwa
babban hargitsi daga ƙasar arewa!
Zai mai da garuruwan Yahuda kufai,
mazaunin diloli.

### *Addu’ar Irmiya*

23 Na sani, ya Ubangiji, cewa ran mutum ba nasa ba ne;
ba mutum ne yake kiyaye takawarsa ba.
24 Ka yi mini gyara, Ubangiji, amma fa da adalci kaɗai

* **10:11** Wannan sashe na wannan aya yana a harshen Arameya ne.

ba cikin fushinka ba,
don kada ka wofinta ni.
25 Ka zuba hasalarka a kan al'umman
da ba su san ka ba,
a kan mutanen da ba sa kira bisa sunanka.
Gama sun cinye Yaƙub;
sun cinye shi gaba ɗaya
suka kuma lalace wurin zamansa.

# 11

*An take alkawari*

1 Ga maganar da ta zo wa Irmiya daga wurin Ubangiji. 2 “Ka saurari zancen
wannan alkawari ka kuma faɗe su ga mutanen Yahuda da kuma waɗanda suke
zaune a Urushalima. 3 Ka faɗa musu cewa ga abin da Ubangiji, Allah na Isra'ila
yana cewa, ‘La'ananne ne wanda bai kula da zancen alkawarin nan ba, 4 zancen
da na umarci kakanni-kakanninku sa'ad da na fitar da su daga Masar, daga cikin
tanderun narkewar ƙarfe.’ Na ce, ‘Ku yi mini biyayya ku kuma aikata kowane abin
da na umarce ku, za ku kuwa zama mutanena, ni kuwa zan zama Allahnku. 5 Sa'an
nan zan cika rantsuwar da na yi wa kakanni-kakanninku, da zan ba su ƙasa mai zub
da madara da kuma zuma' ƙasar da kuka mallaka a yau.”

Sai na amsa na ce, “Amin, Ubangiji.”

6 Sai Ubangiji ya ce mini, “Ka yi shelar dukan maganan nan a biranen Yahuda da
titunan Urushalima duka cewa, ‘Su saurari zancen alkawarin nan, su aikata. 7 Daga
lokacin da na fitar da kakanni-kakanninku daga Masar har yă zuwa yau, na gargaɗe
su sau da sau, ina cewa, “Ku yi mini biyayya.” 8 Amma ba su kasa kunne ko su
saurara ba, a maimako, sai suka bi taurinkai na mugayen zukatansu. Saboda haka
na kawo musu dukan la'anonin alkawarin da na riga na umarce su, su bi amma ba
su kiyaye ba.’ ”

9 Sa'an nan Ubangiji ya ce mini, “Akwai maƙarƙashiya a cikin mutanen Yahuda da
waɗanda suke zaune a Urushalima. 10 Sun koma ga zunuban kakanni kakanninsu,
waɗanda suka ƙi su saurari maganata. Suka bi waɗansu alloli don su bauta musu.
Da gidan Isra'ila da kuma gidan Yahuda duk sun take alkawarin da na yi da kakanni
kakanninsu. 11 Saboda haka ga abin da Ubangiji yana cewa, ‘Zan kawo masifa a kansu
wadda ba za su iya tsere mata ba. Ko da yake suna kuka gare ni, ba zan saurare su
ba. 12 Garuruwan Yahuda da mutanen Urushalima za su tafi su yi kuka ga allolin da
suke ƙona wa turare, amma ba za su taimake su ba sam sa'ad da masifar ta auku.
13 Kuna da alloli masu yawa yadda kuke da garuruwa, ya Yahuda; kuma bagadan da
kuka yi don ƙona turare wa allahn nan Ba'al abin kunya sun yi yawa kamar titunan
Urushalima.’

14 “Kada ka yi addu'a domin wannan mutane ko ka miƙa wani roƙo ko kuka
dominsu, domin ba zan saurara ba sa'ad da suka kira gare ni a lokacin ƙuncinsu.

15 “Mene ne ƙaunatacciyata take yi a haikali
da yake ta yin ƙulle-ƙullen mugayen makircinta tare da mutane masu yawa?
Tsarkakar nama zai iya kawar da hukuncinki?
Sa'ad da kike yin muguntarki
sa'an nan ki yi farin ciki.”*

16 Ubangiji ya kira ki itacen zaitun mai inuwa
kyakkyawa mai 'ya'ya masu kyau.

* **11:15** Ko kuwa Ko tsarkakan nama zai kawar da hukuncinki? Sa'an nan ki yi farin ciki

Amma da ƙugin babbar hadari
zai cinna masa wuta,
rassansa za su kakkarye.
17 UBANGIJI Maɗaukaki, wanda ya dasa ki, ya furta miki masifa, domin gidan Isra'ila
da kuma gidan Yahuda sun aikata mugunta suka kuma tsokane ni in yi fushi ta wurin
ƙona wa Ba'al turare.

*An shirya wa Irmiya maƙarƙashiya*

18 Domin UBANGIJI ya bayyana mini maƙarƙashiyarsu, na santa, gama a wannan
lokaci ya nuna mini abin da suke yi. 19 Na kasance kamar ɗan rago marar faɗa
wanda aka kai mayanka; ban gane cewa sun ƙulla mini maƙarƙashiya, suna cewa,
"Bari mu lalatar da itacen duk da 'ya'yansa;
bari mu datse shi daga ƙasar masu rai,
har da ba za a ƙara tunawa da sunansa ba."
20 Amma, ya UBANGIJI Maɗaukaki, kai da kake yin shari'a da adalci
kake gwada zuciya da kuma tunani,
ka sa in ga sakayyar da za ka yi musu,
gama a gare ka na danƙa maganata.
21 "Saboda haka ga abin da UBANGIJI yana cewa game da mutanen Anatot, waɗanda
suke neman ranka suna kuma cewa, 'Kada ka yi annabci da sunan UBANGIJI in ba haka
za ka mutu a hannunmu' 22 saboda haka ga abin da UBANGIJI Maɗaukaki yana cewa,
'Zan hukunta su. Samarinsu za su mutu ta wurin takobi, 'ya'yansu maza da mata
kuwa ta wurin yunwa. 23 Babu raguwar da za a bar musu, domin zan kawo masifa
a kan mutanen Anatot a shekarar hukuncinsu.' "

# 12

*Damuwar Irmiya*

1 Kullum kai mai adalci ne, ya UBANGIJI,
sa'ad da na kawo ƙara a gabanka.
Duk da haka zan yi magana da kai game da shari'arka.
Me ya sa mugaye suke nasara?
Me ya sa dukan maciya amana suke zama ba damuwa?
2 Ka dasa su, sun kuwa yi saiwa;
sun yi girma suna ba da 'ya'ya.
Kullum sunanka yana a bakinsu
amma kana nesa da zuciyarsu.
3 Duk da haka ka san ni, ya UBANGIJI;
kana ganina ka kuma gwada tunanina game da kai.
Ka ja su kamar tumakin da za a yanka!
Ka ware su don ranar yanka!
4 Har yaushe ƙasar za tă kasance busasshiya*
ciyawar kowane fili ta bushe?
Domin waɗanda suke zaune cikinta mugaye ne,
dabbobi da tsuntsaye sun hallaka.
Ban da haka ma, mutane suna cewa,
"Ba zai ga abin da yake faruwa da mu ba."

*Amsar Allah*

5 "In ka yi tsere da mutane a ƙafa
suka kuma gajiyar da kai,

* **12:4** Ko kuwa ƙasar za tă yi makoki

yaya za ka yi gasa da dawakai?
In ka yi tuntuɓe a lafiyayyiyar ƙasa,†
ƙaƙa za ka yi a kurmin‡ Urdun?
6 ’Yan’uwanka, iyalinka har su ma sun bashe ka;
sun tā da kuka mai ƙarfi a kanka.
Kada ka amince da su,
ko da yake suna faɗa maganganu masu kyau game da kai.

7 “Zan yashe gidana,
in rabu da gādona;
Zan ba da wadda nake ƙauna
a hannuwan abokan gābanta.
8 Gādona ya zama mini
kamar zaki a kurmi.
Yana mini ruri;
saboda haka na ƙi shi.
9 Ashe, gādona bai zama mini
kamar dabbare dabbaren tsuntsu mai cin nama
da sauran tsuntsaye masu cin nama suka kewaye shi da faɗa ba?
Tafi ka tattaro dukan namun jeji;
ka kawo su su ci.
10 Makiyaya masu yawa za su lalace gonar inabina
su tattake gonata;
za su mai da gonata mai kyau
kango marar amfani.
11 Za tă zama kango,
busasshiya da kuma kango a gabana;
ƙasar duka za tă zama kango
domin ba wanda ya kula.
12 A kan dukan tsaunukan nan na hamada
masu hallakarwa za su zo,
gama takobin UBANGIJI zai ci
daga wannan iyaka ƙasa zuwa wancan;
ba wanda zai zauna lafiya.
13 Za su shuka alkama, su girbe ƙayayyuwa;
za su gajiyar da kansu, ba za su kuwa sami kome ba.
Saboda haka ku sha kunyar abin da kuka girbe
saboda zafin fushin UBANGIJI.”
14 Ga abin da UBANGIJI yana cewa, “Game da dukan mugayen maƙwabtana
waɗanda suka ƙwace gādon da na ba wa mutanena Isra’ila kuwa, zan tumɓuke su
daga ƙasashensu zan kuma tumɓuke gidan Yahuda daga cikinsu. 15 Amma bayan na
tumɓuke su, zan sāke jin tausayi in komo da kowannensu zuwa gādonsa da kuma
ƙasarsa. 16 In kuma suka koyi al’amuran mutanena sosai suka kuma yi rantsuwa
da sunana, suna cewa, ‘Muddin UBANGIJI yana raye’ kamar yadda sun taɓa koya wa
jama’ata yin rantsuwa da Ba’al, sa’an nan za su kahu a cikin jama’ata. 17 Amma duk
al’ummar da ba tă saurara ba, zan tumɓuke ta ɗungum in kuma hallaka ta,” in ji
UBANGIJI.

# 13

*Abin ɗamara na lilin*

† **12:5** Ko kuwa In ka dogara a lafiyayyiyar ƙasa ‡ **12:5** Ko kuwa a rigyawar

1 Ga abin da UBANGIJI ya faɗa mini, "Tafi ka sayo abin ɗamara na lilin ka sha
ɗamara da shi, amma kada ka bari yă taɓa ruwa." 2 Saboda haka na sayo abin
ɗamara, yadda UBANGIJI ya umarce ni, na kuwa sha ɗamara da shi.
3 Sai maganar UBANGIJI ta zo mini sau na biyu cewa, 4 "Ka ɗauki abin ɗamara da
ka sayo, wanda ka ɗaura, ka tafi yanzu zuwa Fera* ka ɓoye shi a cikin kogon dutse."
5 Saboda haka na tafi na ɓoye shi a Fera, yadda UBANGIJI ya ce mini.
6 Bayan 'yan kwanaki sai UBANGIJI ya ce mini, "Tafi yanzu zuwa Fera ka ɗauko
abin ɗamara da na ce maka ka ɓoye a can." 7 Sai na tafi Fera da haka na ɗauko abin
ɗamara daga wurin da na ɓoye shi, amma abin ɗamara yanzu ya lalace ya zama ba
shi da amfani sam.
8 Sai maganar UBANGIJI ta zo mini cewa, 9 "Ga abin da UBANGIJI yana cewa, 'Haka
zan lalatar da alfarmar Yahuda da yawan alfarmar Urushalima. 10 Waɗannan
mugayen mutane, waɗanda suka ƙi saurari maganata, waɗanda suka biye wa taurin
zuciyarsu suka bi waɗansu alloli don su bauta su kuma yi musu sujada, za su zama
kamar wannan abin ɗamara gaba ɗaya marasa amfani! 11 Gama kamar yadda abin
ɗamara kan kame gindin mutum tam, haka zan daure dukan gidan Isra'ila da dukan
gidan Yahuda gare ni,' in ji UBANGIJI, 'domin su zama jama'a, da suna, da yabo, da
daraja a gare ni, amma sun ƙi ji.'

*Salkunan ruwan inabi*

12 "Faɗa musu cewa, 'Ga abin da UBANGIJI, Allah na Isra'ila, yana cewa a cika
kowace salkar ruwan inabi da ruwan inabi.' In kuwa suka ce maka, 'Ba mu san
cewa ya kamata a cika kowace salkar ruwan inabi da ruwan inabi ba?' 13 Sai ka
ce musu, 'Ga abin da UBANGIJI yana cewa, zan cika dukan waɗanda suke zama a
ƙasar da buguwa, har ma da sarakunan da suke zama a kursiyin Dawuda, firistoci,
annabawa da dukan waɗanda suke zaune a Urushalima. 14 Zan fyaɗe su a kan juna,
iyaye da 'ya'yansu maza, in ji UBANGIJI. Tausayi ko jinƙai, ko juyayi ba zai hana ni
hallaka su ba.' "

*Barazanar kwashewa zuwa zaman bauta*

15 Ku ji ku kuma saurara,
kada ku yi girman kai,
gama UBANGIJI ya yi magana.
16 Ku ɗaukaka UBANGIJI Allahnku
kafin ya kawo duhu,
kafin ƙafafunku su yi tuntuɓe
a kan tuddai masu duhu.
Za ku sa zuciya ganin haske
amma zai mai da shi duhu mai kauri
ya kuma canja shi zuwa duhu baƙi ƙirin.
17 Amma in ba ku saurara ba,
zan yi kuka a ɓoye
saboda girmankanku;
idanuna za su yi kuka mai zafi,
suna zub da hawaye ƙwarai,
domin zan kwashe garken UBANGIJI zuwa zaman bauta.
18 Ka faɗa wa sarki da kuma mahaifiyar sarauniya cewa,
"Ku sauko daga kursiyinku,
gama rawaninku na ɗaukaka
za su fāɗi daga kawunanku."
19 Za a kulle biranen da suke a Negeb,

* **13:4** Ko kuwa mai yiwuwa Yuferites; haka ma a ayoyi 5-7

kuma babu wanda zai buɗe su.
Za a kwashe dukan Yahuda zuwa zaman bauta,
za a kwashe su tas.

20 Ku tā da idanunku ku ga
waɗanda suke zuwa daga arewa.
Ina garken da aka ba ku
tumakin da kuke taƙama a kai?
21 Me za ku ce sa'ad da UBANGIJI ya naɗa muku
waɗanda ku kanku kuka koya musu a matsayi abokai na musamman?
Ashe, azaba ba za tă auko muku
kamar na mace mai naƙuda ba?
22 In kuma kuka tambaye kanku
"Me ya sa wannan ya faru da mu?"
Wannan kuwa saboda yawan zunubanku ne
ya sa fatarinku ya yage
aka kuma wahalshe jikinku.
23 Mutumin Habasha† zai iya canja launin fatar jikinsa
ko damisa ta canja dabbare dabbarenta?
Ba za ku iya yin alheri
ku da kuka saba da yin mugunta ba.

24 "Zan watsar da ku kamar yayin
da iskar hamada take hurawa.
25 Rabonku ne wannan,
sashen da na auka muku,"
in ji UBANGIJI
"domin kun manta da ni
kuka kuma dogara ga allolin ƙarya.
26 Zan kware fatarinku sama ya rufe fuskarku
don a iya ga tsiraicinku
27 zinace zinacenku da haniniya kamar dawakai,
karuwancinku na bankunya!
Na ga ayyukanku na banƙyama
a kan tuddai da kuma a filaye.
Kaitonki, ya Urushalima!
Har yaushe za ki ci gaba da rashin tsarki?"

# 14

### *Fari, yunwa da takobi*

1 Ga maganar UBANGIJI da ta zo wa Irmiya game da fări cewa,
2 "Yahuda tana makoki
biranenta suna fama;
suna kuka saboda ƙasar,
kuka kuma tana tasowa daga Urushalima.
3 Manyan mutane suna aika bayinsu su ɗebo ruwa
a maɓulɓulai amma babu ruwa.
Suka dawo da tulunansu haka nan;
da kunya da kuma ƙasƙanci, da kawunansu a rufe.
4 Kasa ta tsattsage

† **13:23** Da Ibraniyanci Mutumin Kush (mai yiwuwa mutum daga yankin Bisa na Nilu).

saboda babu ruwan sama a ƙasar;
manoma sun sha kunya
suka kuma rufe kawunansu.
5 Har barewa a kurmi ma
ta gudu ta bar ʼyaʼyan da ta haihu sababbi
saboda babu ciyawa.
6 Jakan jeji suna tsaye a kan tuddai
suna haki kamar diloli;
idanunsu sun kāsa gani
saboda rashin makiyaya."

7 Ko da yake zunubanmu suna ba da shaida a kanmu,
Ya UBANGIJI, ka yi wani abu saboda sunanka.
Gama jan bayanmu ya yi yawa;
mun yi maka zunubi.
8 Ya kai, Sa Zuciyar Isra'ila,
Mai Cetonsa a lokutan wahala,
me ya sa kake yi kamar baƙo a ƙasar,
kamar matafiyi wanda yake shirya wuri don yă kwana gari ya waye ya wuce?
9 Me ya sa kake yi kamar mutumin da aka far masa kwasam ba zato,
kamar jarumi marar ƙarfin ceto?
Kana a cikinmu, ya UBANGIJI,
da sunanka ake kiranmu;
kada ka yashe mu!
10 Ga abin da UBANGIJI ya ce game da wannan mutane,
"Suna son yawace-yawace ƙwarai;
ba sa hana ƙafafunsu yawo.
Saboda haka UBANGIJI bai yarda da su ba;
yanzu zai tuna da muguntarsu
zai kuma hukunta su saboda zunubansu."
11 Sa'an nan UBANGIJI ya ce mini, "Kada ka yi addu'a domin zaman lafiyar mutanen
nan. 12 Ko da yake suna azumi, ba zan saurari kukansu ba, ko da yake suna miƙa
hadayun ƙonawa da hadayun gari, ba zan yarda da su ba. A maimako zan hallaka
su da takobi, yunwa da annoba."
13 Amma na ce, "A, UBANGIJI Mai Iko Duka, annabawa sun riƙa ce musu, 'Ba za
ku ga takobi ko ku yi fama da yunwa ba. A maimako, zan ba ku madawwamiyar
salama.' "
14 Sai UBANGIJI ya ce mini, "Annabawa suna ta annabcin ƙarya da sunana. Ban aike
su ba, ban kuma naɗa su ba, ban yi musu magana ba. Suna muku annabci wahayin
ƙarya, suna muku duba marar amfani, suna bautar gumaka suna kuma bayyana
tunanin kansu ne. 15 Saboda haka, ga abin da UBANGIJI ya ce game da annabawan
da suke annabci da sunana. Ban aike su ba, duk da haka suna cewa, 'Babu takobi
ko yunwar da zai taɓa wannan ƙasa.' Waɗannan annabawa takobi da yunwa za
su hallaka su. 16 Mutanen da suke musu annabcin kuwa za a kore su zuwa titunan
Urushalima saboda yunwa da kuma takobi. Babu wanda zai binne su, ko ya binne
matansu, ko 'ya'yansu maza da mata. Zan aukar musu da masifar da ya dace da su.
17 "Ka yi musu wannan magana,
" 'Bari idanuna su yi ta zub da hawaye
dare da rana kada su daina;
saboda 'yata budurwa, mutanena,
sun sha wahalar babban rauni,
an yi musu bugu mai ragargazawa.

18 In na shiga cikin ƙasar,
na ga waɗanda takobi ya kashe;
in na shiga cikin birni,
na ga waɗanda suke fama da yunwa.
Da Annabi da firist duk
sun tafi ƙasar da ba su sani ba.' "

19 Ka ƙi Yahuda ɗungum ke nan?
Kana ƙyamar Sihiyona ne?
Me ya sa ka buge mu
don kada mu warke?
Mun sa zuciya ga salama
babu abin alherin da ya zo,
mun sa rai ga lokacin warkarwa
amma sai ga razana.
20 Ya UBANGIJI, mun gane da muguntarmu
da kuma laifin kakanninmu;
tabbatacce mun yi maka zunubi.
21 Saboda sunanka kada ka ƙi mu;
kada ka ƙasƙantar da kursiyoyinka mai ɗaukaka.
Ka tuna da alkawarinka da mu
kada ka tā da shi.
22 Akwai wani daga cikin gumaka marasa amfani na al'ummai da ya kawo ruwan sama?
Sararin sama kansu sukan yi yayyafi?
A'a, kai ne, ya UBANGIJI Allahnmu.
Saboda haka sa zuciyarmu tana a kanka,
gama kai ne kake yi wannan duka.

# 15

1 Sai UBANGIJI ya ce mini, "Ko da Musa da Sama'ila za su tsaya a gabana, zuciyata
ba za tă komo ga mutanen nan ba. Ka kore su daga gabana! Su tafi! 2 In kuma suka
tambaye ka, 'Ina za mu tafi?' Sai ka faɗa musu, 'Ga abin da UBANGIJI yana cewa,
" 'Waɗanda aka ƙaddara ga mutuwa, ga mutuwa za su;
waɗanda aka ƙaddara ga takobi, ga takobi za su;
waɗanda aka ƙaddara ga yunwa, ga yunwa za su;
waɗanda aka ƙaddara ga zaman bauta, ga zaman bauta za su.'
3 "Zan aika musu da iri masu hallakarwa guda huɗu," in ji UBANGIJI, "takobi zai
kashe, karnuka za su kwashe, tsuntsaye da namun jeji kuma su cinye su kuma
hallaka. 4 Zan sa su zama abin ƙyama ga dukan mulkokin duniya saboda abin da
Manasse ɗan Hezekiya sarkin Yahuda ya aikata a Urushalima.
5 "Wa zai ji tausayinki, ya Urushalima?
Wa zai yi makoki dominki?
Wa zai dakata ya tambayi lafiyarki?
6 Kin ƙi ni," in ji UBANGIJI.
"Ki ci gaba da ja da baya.
Ta haka zan ɗibiya hannuwana a kanki in hallaka ki;
ba zan ƙara nuna miki jinƙai ba.
7 Zan sheƙe ki da abin sheƙewa
a ƙofofin birnin ƙasar.
Zan kawo baƙin ciki da hallaka a kan mutanena,
gama ba su canja hanyoyinsu ba.

8 Zan ƙara yawan gwaurayensu
su fi yashin teku yawa.
Da tsakar rana zan kawo mai hallakarwa
a kan iyaye mata na samarinsu;
farat ɗaya zan kawo musu
wahala da razana.
9 Mahaifiya ’ya’ya bakwai za tă suma
ta ja numfashinta na ƙarshe.
Ranarta zai fāɗi tun lokacin bai yi ba;
za tă sha kunya a kuma wulaƙanta ta.
Zan sa a kashe raguwa da takobi
a gaban abokan gābansu,”
in ji UBANGIJI.

10 Kaitona, mahaifiyata, da kika haife ni,
mutumin da dukan ƙasa take faɗa take kuma gardama da shi!
Ban ba da bashi ko in ci bashi ba,
duk da haka kowa yana zagina.
11 UBANGIJI ya ce,
“Tabbatacce zan cece ka don alheri;
tabbatacce zan sa abokan gābanka su yi roƙo gare ka
a lokacin masifa da kuma lokacin wahala.

12 “Mutum zai iya karye ƙarfe
ƙarfe daga arewa, ko tagulla?

13 “Dukiyarku da arzikinku
zan ba da su ganima, babu tara,
saboda duka zunubanku
ko’ina a ƙasar.
14 Zan bautar da ku ga abokan gābanku
a ƙasar da ba ku sani ba,
gama fushina zai yi ƙuna kamar wuta
da za tă yi ƙuna a kanku.”

15 Ka gane, ya UBANGIJI;
ka tuna da ni ka kuma lura da ni.
Ka yi mini ramuwa a kan masu tsananta mini.
Cikin jimirinka, kada ka ɗauke ni;
ka tuna yadda na sha zagi saboda kai.
16 Sa’ad da maganganunka suka zo, na cinye su;
suka zama abin farin ciki zuciyata kuma ta yi murna,
gama ana kirana da sunanka,
Ya UBANGIJI Allah Maɗaukaki.
17 Ban taɓa zauna a cikin ’yan tawaye ba,
ban taɓa yi murna da su ba;
na zauna ni kaɗai domin hannunka yana a kaina
ka kuma sa na cika da haushi.
18 Me ya sa wahalata ba ta ƙarewa
mikina kuma ba ya warkuwa?
Za ka zama mini kamar rafi mai yaudara ne,
kamar maɓulɓulan da ta kafe ne?

19 Saboda haka ga abin da UBANGIJI yana cewa,
"In ka tuba, zan maido da kai
don ka bauta mini;
in ka ambaci maganganu masu kyau, ba marasa kyau ba,
za ka zama kakakina.
Bari wannan mutane su juyo gare ka,
amma kada ka juye gare su.
20 Zan mai da kai katanga ga wannan mutane,
katanga mai ƙarfi na tagulla;
za su yi yaƙi da kai
amma ba za su yi nasara a kanka ba,
gama ina tare da kai
don in kuɓutar in kuma cece ka,"
in ji UBANGIJI.
21 "Zan cece ka daga hannuwan mugaye
in ɓamɓare ka daga hannun marasa tausayi."

# 16

*Ranar masifa*

1 Sai maganar UBANGIJI ta zo mini cewa, 2 "Kada ka yi aure ka haifi 'ya'ya maza da
mata a wannan wuri." 3 Gama ga abin da UBANGIJI yana cewa game da 'ya'ya maza
da matan da aka haifa a wannan ƙasa da kuma game da matan da suke iyayensu da
suke mazan da iyayensu. 4 "Za su mutu da muguwar cuta. Ba za a yi kuka dominsu
ba, ba kuwa za a binne su ba, amma za a bar su a juji. Takobi da yunwa ne za
su hallaka su, gawawwakinsu za su zama abincin tsuntsayen sararin sama da kuma
namun jeji na duniya."
5 Gama ga abin da UBANGIJI yana cewa, "Kada ka shiga gidan da akwai abincin
makoki; kada ka tafi ka yi makoki ko ka nuna juyayi, domin na janye albarkata,
ƙaunata da tausayina daga wannan mutane," in ji UBANGIJI. 6 "Manya da ƙanana
duka za su mutu a wannan ƙasa. Ba za a binne su ba, ba kuwa za a yi makokinsu
ba, kuma ba wanda zai tsaga kansa ko ya aske kansa saboda su. 7 Ba wanda zai ba
da abinci don yă ta'azantar da waɗanda suke makoki saboda matattu, kai, ko saboda
mahaifi ko mahaifiya ma ba kuwa wani da zai ba da abin sha don yă ta'azantar da
su.
8 "Kada kuma ka shiga gidan da ake biki ka zauna don ci da sha. 9 Gama ga abin da
UBANGIJI Maɗaukaki, Allah na Isra'ila, yana cewa a idanunka da kuma a kwanakinka
zan kawo ƙarshen muryar farin ciki da murna da kuma muryoyin amarya da ango
a wannan wuri.
10 "Sa'ad da ka faɗa wa waɗannan mutane wannan duka suka kuma tambaye ka,
'Me ya sa UBANGIJI ya ƙaddara irin wannan babban masifa a kanmu? Wace mugunta
muka yi? Wane zunubi muka aikata wa UBANGIJI Allahnmu?' 11 Sai ka ce musu,
'Wannan ya zama haka domin kakanninku sun rabu da ni,' in ji UBANGIJI, 'suka bi
waɗansu alloli suka kuma bauta musu. Suka rabu da ni, ba su kuwa kiyaye dokata
ba. 12 Amma kun yi laifi fiye da kakanninku. Duba yadda kowannenku yana bin
taurin muguwar zuciyarsa a maimakon yin mini biyayya. 13 Saboda haka zan fitar
da ku daga wannan ƙasa zuwa wata ƙasar da ku da kakanninku ba ku taɓa sani ba,
a can kuwa za ku bauta wa waɗansu alloli dare da rana, gama ba zan nuna muku
tagomashi ba.'
14 "Amma fa, kwanaki suna zuwa," in ji UBANGIJI, "da mutane ba za su ƙara cewa,
'Muddin UBANGIJI yana raye, wanda ya fitar da Isra'ilawa daga Masar,' 15 amma za
su ce, 'Muddin UBANGIJI yana raye, wanda ya fitar da Isra'ilawa daga ƙasar arewa da

kuma daga dukan ƙasashe da ya kora su.' Gama zan komo da su zuwa ƙasar da na ba wa kakanninsu.
16 "Amma yanzu zan aiko a kira masunta masu yawa su zo," in ji UBANGIJI, "za su kuma kama su. Bayan wannan zan aiko a kira mafarauta su zo, su farauce su daga kowane dutse da tudu da kuma daga kogwannin duwatsu.
17 Idanuna suna a kan dukan hanyoyinsu; ba a ɓoye suke daga gare ni, kuma zunubansu ba a ɓoye suke a idanuna ba.
18 Zan riɓaɓɓanya sakayyar da zan yi musu saboda muguntarsu da zunubinsu, domin sun ƙazantar da ƙasata da ƙazantattun gumakansu marasa rai, suka kuma cika abin gādona da gumakansu na banƙyama."

19 Ya UBANGIJI, ƙarfina da katangana,
mafakata a lokacin damuwa,
gare ka al'ummai za su zo
daga iyakokin duniya su ce,
"Kakanninmu ba su mallaki kome ba sai allolin ƙarya,
gumakan banza da ba su yi musu amfani ba.
20 Mutane kan yi allolinsu ne?
I, amma waɗannan ba alloli ba ne!"

21 "Saboda haka zan koya musu
a wannan lokaci zan koya musu
ikona da ƙarfina.
Sa'an nan za su sani
cewa sunana UBANGIJI ne.

# 17

1 "An rubuta zunubin Yahuda da alƙalamin ƙarfe,
an rubuta da tsinin dutse,
a kan allunan zukatansu
da kuma a kan ƙahonin bagadansu.
2 Har 'ya'yansu ma sun tuna
bagadansu da ginshiƙan Asheransu
kusa da itatuwa masu duhuwa
da kuma a kan tuddai masu tsayi.
3 Dutsena a ƙasar
da* dukiyarku na ƙasar da dukan arzikinku
za a ba da su ganima,
tare da masujadanku na kan tuddai,
saboda zunubi ko'ina a ƙasarku.
4 Saboda laifinku za ku rasa
gādon da na ba ku.
Zan bautar da ku ga abokan gābanku
a ƙasar da ba ku sani ba,
domin kun husata ni,
zai kuwa ci har abada."
5 Ga abin da UBANGIJI yana cewa,
"La'ananne ne mutumin da yake dogara ga mutum,
wanda ya dogara ga jiki don ƙarfi
wanda kuma zuciyarsa ta juya wa UBANGIJI baya.
6 Zai zama kamar ɗan kurmi a ƙasar da take kango;
ba za su ga arziki sa'ad da ya zo ba.

* **17:3** Ko kuwa tuddai 3 da duwatsun ƙasar. Naku

Za su zauna a busassun wuraren hamada,
a cikin ƙasar gishiri inda ba kowa.

7 “Amma mai albarka ne mutumin da yake dogara ga UBANGIJI,
wanda ƙarfin halinsa yana daga UBANGIJI.
8 Za su zama kamar itacen da aka dasa kusa da ruwa
wanda ya miƙa saiwoyinsa zuwa cikin rafi.
Ba ya jin tsoro sa’ad da zafi ya zo;
ganyayensa kullum kore suke.
Ba shi da damuwa a shekarar fări
ba ya taɓa fasa ba da ’ya’ya.”

9 Zuciya ta fi kome ruɗu
ta fi ƙarfin warkewa.
Wa zai iya gane ta?

10 “Ni UBANGIJI nakan bincike zuciya
in gwada tunani,
don in sāka wa kowane mutum bisa ga halinsa,
bisa ga ayyukansa.”

11 Kamar makwarwar da ta kwanta a kan ƙwan da ba ita ta zuba ba
haka yake da mutumin da ya sami arziki a hanyar da ba daidai ba.
A tsakiyar rayuwarsa za su rabu da shi,
a ƙarshe kuma zai zama wawa.

12 Kursiyi mai daraja, da aka ɗaukaka tun daga farko,
shi ne wuri mai tsarkinmu.
13 Ya UBANGIJI, sa zuciyar Isra’ila,
duk waɗanda suka rabu da kai za su sha kunya.
Waɗanda suka juya maka baya za a rubuta su a ƙura
domin sun yashe UBANGIJI,
maɓulɓular ruwan rai.

14 Ka warkar da ni, ya UBANGIJI, zan kuwa warke;
ka cece ni zan kuwa cetu,
gama kai ne nake yabo.
15 Sun riƙa ce mini, “Ina maganar UBANGIJI take?
Bari tă cika yanzu!”
16 Ban gudu zaman mai yin maka kiwo ba;
ka sani ban marmarin ranan nan ta masifa ba.
Abin da ya fito daga leɓunana kuwa, a bayyane suke gare ka.
17 Kada ka zama mini abin razana;
kai ne mafakata a ranar masifa.
18 Bari masu tsananta mini su sha kunya,
amma ka kiyaye ni daga shan kunya;
bari su tsorata,
amma ka kiyaye ni da razana.
Ka kawo musu ranar masifa;
ka hallaka su da hallaka riɓi biyu.

### *Kiyaye Asabbaci da tsarki*

19 Ga abin da Ubangiji ya ce mini, “Ka je ka tsaya a ƙofar mutane, inda sarakunan
Yahuda sukan shiga su fita; ka tsaya kuma a dukan sauran ƙofofin Urushalima. 20 Ka
ce musu, ‘Ku ji maganar Ubangiji, ku sarakunan Yahuda, da dukan mutanen Yahuda
da dukan mazaunan Urushalima waɗanda suke bi ta waɗannan ƙofofi. 21 Ga abin da
Ubangiji yana cewa, ku yi hankali kada ku ɗauki kaya a ranar Asabbaci ko ku shigar
da shi ta ƙofofin Urushalima. 22 Kada ku fitar da kayan gidajenku ko ku yi wani aiki a
ranar Asabbaci mai tsarki, yadda na umarci kakanni-kakanninku. 23 Duk da haka ba
su saurara ba, ba su kuwa mai da hankali ba; suka taurare ba su kuwa saurara ko su
karɓi horo ba. 24 Amma in kuka yi hankali kuka yi mini biyayya, in ji Ubangiji, ba ku
kuwa shigar da kaya ta ƙofofi a ranar Asabbaci ba, amma kuka kiyaye ranar Asabbaci
da tsarki ba tare da yin wani aiki a cikinta ba, 25 sa’an nan sarakuna da suke zama
a kursiyin Dawuda za su shiga ta ƙofofin wannan birni tare da fadawansu. Su da
fadawansu za su shiga a kan kekunan yaƙi da kuma a kan dawakai, mutanen Yahuda
suna musu rakiya tare da waɗanda suke zaune a Urushalima, wannan birni kuwa za
tă kasance da mazauna har abada. 26 Mutane za su zo daga garuruwan Yahuda da
ƙauyukan kewaye da Urushalima, daga iyakar Benyamin da gindin tuddan yamma,
daga ƙasar tudu da kuma Negeb, suna kawo hadayun ƙonawa da hadayun gari,
sadakokin turare da na godiya zuwa gidan Ubangiji. 27 Amma in ba ku yi mini biyayya
ba, ba ku kiyaye ranar Asabbaci da tsarki ba, kuka ɗauki wani kaya yayinda kuke
shiga ƙofofin Urushalima a ranar Asabbaci, to, sai in cinna wa ƙofofin Urushalima
wutar da ba a iya kashewa, tă cinye kagaranta.’ ”

# 18

### *A gidan mai ginin tukwane*

1 Ga maganar da ta zo wa Irmiya daga wurin Ubangiji. 2 “Ka gangara zuwa gidan
mai ginin tukwane, a can zan ba ka saƙona.” 3 Sai na gangara zuwa gidan mai ginin
tukwane, na gan shi yana aiki a na’urar ginin tukwanen. 4 Amma tukunyar da yake
ginawa ta lalace a hannuwansa, sai mai ginin tukwanen ya sāke gina wata tukunya
dabam, yana gyara ta yadda ya ga dama.

5 Sai maganar Ubangiji ta zo mini cewa, 6 “Ya gidan Isra’ila, ashe, ba zan yi da ku
yadda mai ginin tukwanen nan yake yi ba?” In ji Ubangiji. “Kamar yumɓu a hannun
mai ginin tukwane, haka kuke a hannuna, ya gidan Isra’ila. 7 A duk lokacin da na
yi shela cewa za a tumɓuke, a kakkarya a kuma hallaka wata al’umma ko mulki,
8 in wannan al’ummar da na yi wa gargaɗi ta tuba daga muguntarta, sai in janye in
kuma fasa kawo mata masifar da na yi niyya aukar mata. 9 In kuma wani lokaci na
yi shela cewa za a gina wata al’umma ko mulki a kuma kafa ta, 10 in ta yi mugunta a
gabana ba tă kuwa yi mini biyayya ba, sai in janye alherin da na yi niyya in yi mata.

11 “Yanzu fa, sai ka faɗa wa mutanen Yahuda da waɗanda suke zaune a Urushalima,
‘Ga abin da Ubangiji yana cewa ga shi! Ina shirya muku masifa ina ƙirƙiro dabara
a kanku. Saboda haka ku juya daga mugayen hanyoyinku, kowannenku, ku canja
hanyoyinku da kuma ayyukanku.’ 12 Amma za su amsa su ce, ‘Ba amfani. Za mu ci
gaba da shirye-shiryenmu; kowannenmu zai bi taurin muguwar zuciyarsa.’ ”

13 Saboda haka ga abin da Ubangiji yana cewa,

“Ku tattambaya a cikin al’ummai.
    Wa ya taɓa jin irin wannan abu?
Budurwa Isra’ila ta yi mugun abu
    mafi banƙyama.
14 Dusar ƙanƙarar Lebanon
    ta taɓa rabuwa da kan duwatsun Lebanon?
Ruwan mai sanyinsa daga rafuffukansa masu nesa

sun taɓa daina gudu?
15 Duk da haka mutanena sun manta da ni;
sun ƙone turare wa gumaka marasa amfani,
waɗanda suka sa su tuntuɓe a al'amuransu
a hanyoyin dā.
Sun sa suka yi tafiya a ɓarayin hanyoyi
a hanyoyin da ba a gina ba.
16 Kasarsu za tă zama kufai,
abin reni har abada;
dukan waɗanda suka wuce za su yi mamaki
su kaɗa kai.
17 Kamar iska daga gabas
zan warwatsa su a gaban abokan gābansu;
zan juya musu bayana, ba zan nuna musu fuskata ba
a ranar masifarsu."
18 Suka ce, "Zo mu shirya wa Irmiya maƙarƙashiya; gama koyarwar doka da firist
ya yi ba za tă ɓace ba, haka ma shawara daga mai hikima da kuma magana daga
annabawa. Saboda haka ku zo, mu fāɗa masa da harsunanmu kada mu saurari wani
abin da zai faɗa."

*Addu'ar Irmiya*

19 Ka saurare ni, ya UBANGIJI
ka ji abin da masu zargina suke cewa!
20 Ya kamata a sāka wa alheri da mugunta?
Duk da haka sun haƙa mini rami.
Ka tuna cewa na tsaya a gabanka
na kuma yi magana a madadinsu
don ka janye fushinka daga gare su.
21 Saboda haka ka kawo wa 'ya'yansu yunwa;
ka miƙa su ga ikon takobi.
Bari matansu su zama marasa 'ya'ya da gwauraye;
bari a kashe mazansu,
a kuma kashe samarinsu da takobi a yaƙi.
22 Bari a ji kuka daga gidajensu
sa'ad da ka kawo masu hari a kansu farat ɗaya,
gama sun haƙa rami don su kama ni
suka kuma kafa tarko wa ƙafafuna.
23 Amma Ya UBANGIJI,
ka san duk maƙarƙashiyarsu, na neman su kashe ni.
Kada ka gafarta musu laifofinsu
ko ka shafe zunubansu daga gabanka.
Bari a tumɓuke su a gabanka;
ka yi da su sa'ad da kake fushi.

# 19

1 Ga abin da UBANGIJI yana cewa, "Tafi ka sayo tulu a wurin mai ginin tukwane.
Ka ɗauki waɗansu dattawan jama'a da kuma na firistoci 2 ku fita zuwa Kwarin Ben
Hinnom, kusa da mashigin Kofar Kasko. A can ka furta maganganun da na faɗa
maka, 3 ka ce, 'Ku ji maganar UBANGIJI, ya sarakunan Yahuda da kuma mutanen
Urushalima. Ga abin da UBANGIJI Maɗaukaki, Allah na Isra'ila, yana cewa ku saurara!
Zan kawo masifa a wannan wuri, wanda duk ya ji, kunnuwansa za su kaɗa. 4 Gama
sun yashe ni suka kuma mai da wannan wuri ya zama na baƙin alloli; sun ƙone

hadayu a cikinsa wa allolin da ko su ko kakanninsu ko sarakunan Yahuda ba su taɓa
sani ba, suka kuma cika wannan wuri da jini marasa laifi. 5 Suka gina masujadai na
kan tudu na Ba'al don su ƙona 'ya'yansu maza a cikin wuta a matsayin hadaya ga
Ba'al abin da ban umarta ba, ban ambata ba, bai kuma zo mini ba. 6 Saboda haka ku
lura, kwanaki suna zuwa, in ji UBANGIJI, sa'ad da mutane ba za su ƙara ce da wannan
wuri Tofet ko Kwarin Ben Hinnom ba, amma za su ce da shi Kwarin Kisa.
7 " 'A wannan wuri zan lalace* dabarun Yahuda da na Urushalima. Zan sa a kashe
su da takobi a gaban abokan gābansu, a hannuwan waɗanda suke neman ransu,
zan kuma ba da gawawwakinsu su zama abinci ga tsuntsayen sararin sama da kuma
namun jeji. 8 Zan ragargazar da wannan birni in mai da shi abin reni, duk wanda ya
wuce zai yi mamaki ya kuma yi tsaki saboda dukan masifunsa. 9 Zan sa su ci naman
'ya'yansu maza da mata, za su kuma ci naman juna a lokacin damuwar ƙawanya da
abokan gāban da suke neman ransu za su yi musu.'
10 "Sa'an nan ka fasa tulun yayinda waɗanda suka tafi tare da kai suna duba,
11 ka kuma ce musu, 'Ga abin da UBANGIJI Maɗaukaki yana cewa zan farfasa wannan
al'umma da wannan birni kamar yadda aka farfasa wannan tulu mai ginin tukwane
ba kuwa zai gyaru ba. Za a binne matattu a Tofet har sai ba sauran wuri. 12 Ga abin
da zan yi wa wannan wuri da waɗanda suke zaune a nan, in ji UBANGIJI. Zan mai
da wannan birni kamar Tofet. 13 Gidaje a Urushalima da waɗannan na sarakunan
Yahuda za su ƙazantu kamar wannan wuri, Tofet, dukan gidajen da suke ƙone turare
a kan rufi wa duk rundunan taurari suna kuma zuba hadayun sha ga sauran alloli.' "
14 Sa'an nan Irmiya ya komo daga Tofet, inda UBANGIJI ya aike shi don yǎ yi annabci,
ya tsaya a filin haikalin UBANGIJI ya ce wa mutane duka, 15 "Ga abin da UBANGIJI
Maɗaukaki, Allah na Isra'ila, yana cewa, 'Ku saurara! Zan kawo wa wannan birni
da ƙauyukan da suke kewayensa kowace masifar da na furta a kansu, domin sun yi
taurinkai, ba su kuwa saurari maganata ba.' "

# 20

### *Irmiya da Fashhur*

1 Da firist nan Fashhur ɗan Immer, babban ma'aikaci a cikin haikalin UBANGIJI, ya
ji Irmiya yana annabcin waɗannan abubuwa, 2 sai ya sa aka yi wa Irmiya dūka aka
kuma sa shi a turu a Kofar Bisa na Benyamin a haikalin UBANGIJI. 3 Kashegari, sa'ad
da Fashhur ya fitar da shi daga turu, sai Irmiya ya ce masa, "UBANGIJI ba zai kira
ka Fashhur ba, amma ya ba ka suna Magor-Missabib.* 4 Gama ga abin da UBANGIJI
yana cewa, 'Zan maishe ka abin razana ga kanka da kuma ga dukan abokanka; da
idanunka za ka gan takobin abokan gāba yana kashe su. Zan miƙa Yahuda duka
ga sarkin Babilon, wanda zai kwashe su zuwa Babilon ya kuma kashe su da takobi.
5 Zan ba wa abokan gābansu dukan dukiyar wannan birni dukan amfaninsa, dukan
abubuwa masu daraja na sarakunan Yahuda. Za su kwashe su ganima su kai su
Babilon. 6 Kai kuma Fashhur, da dukan waɗanda suke a gidanka za ku tafi zaman
bauta a Babilon. A can za ku mutu a kuma binne ku, da kai da dukan abokanka
waɗanda ka yi musu annabce-annabcen ƙarya.' "

### *Damuwar Irmiya*

7 Ya UBANGIJI, ka ruɗe† ni, na kuwa ruɗu;
ka fi ni ƙarfi, ka kuwa yi nasara.
Na zama abin dariya dukan yini;
kowa yana yi mini ba'a.

---

* **19:7** Ibraniyanci na lalace ya yi kamar Ibraniyanci na tulu (dubi ayoyi 1 da 10). * **20:3** Magor-Missabib yana nufin razana ta kowace fuska. † **20:7** Ko kuwa rarrashe

8 Duk sa'ad da na yi magana, nakan tā da murya
ina furta hargitsi da hallaka.
Haka maganar UBANGIJI ta kawo mini
zagi da reni dukan yini.
9 Amma in na ce, "Ba zan ambace shi ba
ba zan ƙara yin magana da sunansa ba,"
sai in ji maganarsa a cikina kamar wuta,
wutar da aka kulle a ƙasusuwana.
Na gaji da danne ta a cikina;
tabbatacce ba zan iya ba.
10 Na ji mutane da yawa suna raɗa cewa,
"Razana ta kowace fuska!
Mu kai kararsa! Bari mu kai kararsa!"
Dukan abokaina
suna jira in yi tuntuɓe, suna cewa,
"Mai yiwuwa a ruɗe shi;
sai mu yi nasara a kansa
mu ɗau fansa a kansa."
11 Amma UBANGIJI yana tare da ni kamar babban jarumi;
saboda haka masu tsananta mini za su yi tuntuɓe ba kuwa za su yi nasara ba.
Za su fāɗi su kuma sha mummunar kunya;
ba za a taɓa manta da rashin bangirmansu ba.
12 Ya UBANGIJI Maɗaukaki, kai da kake gwada adali
kana bincika zuciya duk da tunani,
bari in ga sakayyarka a kansu,
gama a gare ka na miƙa damuwata.

13 Ku rera ga UBANGIJI!
Ku yabi UBANGIJI!
Ya kuɓutar da ran mabukaci
daga hannuwan mugaye.

14 La'ananniya ce ranar da aka haife ni!
Kada ranar da mahaifiyata ta haife ni ta zama mai albarka!
15 La'ananne ne mutumin da ya kawo wa mahaifina labari,
wanda ya sa shi ya yi murna cewa, "An haifa maka yaro, ɗa namiji!"
16 Bari mutumin ya zama kamar garuruwan
da UBANGIJI ya tumɓuke ba tausayi.
Bari yǎ ji kuka da safe
kururuwan yaƙi kuma da tsakar rana.
17 Gama bai kashe ni a cikin ciki ba,
da ma ya sa cikin mahaifiyata ya zama kabarina,
cikinta ya fadada har abada.
18 Me ya sa na ma fito daga cikin ciki
in ga wahala da baƙin ciki
in kuma ƙare kwanakina da kunya?

# 21

*Allah ya ƙi amsa roƙon Zedekiya*

1 Magana ta zo wa Irmiya daga UBANGIJI sa'ad da Sarki Zedekiya ya aiki Fashhur
ɗan Malkiya da firist Zefaniya ɗan Ma'asehiya gare shi. Suka ce masa, 2 "Yanzu ka

roƙi mana UBANGIJI saboda Nebukadnezzar[*] sarkin Babilon yana kawo mana yaƙi.
Wataƙila UBANGIJI zai yi mana waɗansu abubuwa banmamaki kamar a lokacin baya
don yă janye daga gare mu.”
3 Amma Irmiya ya amsa musu ya ce, “Ku faɗa wa Zedekiya cewa, 4 ‘Ga abin
da UBANGIJI, Allah na Isra’ila, yake cewa ina shirin juya kayan yaƙin da suke a
hannuwanka a kanka, waɗanda kake amfani don ka yaƙi sarki Babilon da kuma
Babiloniyawa[†] waɗanda suka kewaye katangar birnin, zan kuwa tsiba kayan yaƙinka
a tsakiyar birnin nan. 5 Ni da kaina zan yi yaƙi da kai da miƙaƙƙen hannu mai ƙarfi
cikin fushi da hasala mai girma. 6 Zan kashe waɗanda suke zaune a wannan birni,
mutane da dabbobi za su kuwa mutu da muguwar annoba. 7 Bayan wannan, in ji
UBANGIJI, zan ba da Zedekiya sarkin Yahuda, fadawansa da kuma mutanen wannan
birni waɗanda suka tsira daga annoba, takobi da kuma yunwa, ga Nebukadnezzar
sarkin Babilon da kuma ga abokan gābansu waɗanda suke neman ransu. Zai kashe
su da takobi; ba zai ji tausayinsu ko ya yi musu jinƙai ko ya yi juyayinsu ba.’
8 “Bugu da ƙari, ka faɗa wa mutanen cewa, ‘Ga abin da UBANGIJI yana cewa, ga shi
na sa a gabanku hanyar rai da hanyar mutuwa. 9 Duk wanda ya zauna a wannan
birni zai mutu ta takobi, yunwa ko annoba. Amma duk wanda ya fita ya miƙa kansa
ga Babiloniyawa waɗanda suka kewaye ku zai rayu; zai kuɓutar da ransa. 10 Na
ƙudura in yi wa wannan birni lahani ba alheri ba, in ji UBANGIJI. Za a ba da shi a
hannuwan sarki Babilon, zai kuwa hallaka shi da wuta.’
11 “Ban haka ma, ka faɗa wa gidan sarauta na Yahuda cewa, ‘Ku saurari maganar
UBANGIJI; 12 Ya gidan Dawuda ga abin da UBANGIJI yana cewa,

“ ‘Ku yi gaskiya kowace safiya;
ku kuɓuta daga hannun mai danniya
wannan da aka yi wa fashi
in ba haka ba hasalata za tă sauka ta kuma ci kamar wuta
saboda muguntar da kuka aikata
za tă ci babu wanda zai kashe ta.
13 Ina gāba da ku, mazaunan Urushalima,
ku da kuke zama a bisa wannan kwari
kan dutsen da yake a fili,
in ji UBANGIJI
ku da kuke cewa, “Wa zai iya yaƙe mu?
Wa zai iya shiga mafakarmu?”
14 Zan hukunta ku gwargwadon ayyukanku,
in ji UBANGIJI.
Zan sa wuta a kurminku
da za tă cinye kome da yake kewaye da ku.’ ”

# 22

*Hukunci a kan mugayen sarakunan Yahuda*

1 Ga abin da UBANGIJI yana cewa, “Ka gangara zuwa fadan sarkin Yahuda ka yi
shelar wannan saƙo a can ka ce, 2 ‘Ka ji maganar UBANGIJI, ya sarkin Yahuda, kai da
kake zaune kan gadon sarautar Dawuda, kai, da fadawanka da mutanenka waɗanda
suke shiga ta waɗannan ƙofofi. 3 Ga abin da UBANGIJI yana cewa, ka yi abin da
yake gaskiya da kuma daidai. Ka kuɓutar da wannan da aka yi masa ƙwace daga
hannun mai zaluntarsa. Kada ka yi abin da ba daidai ba ko ka cuci baƙo, maraya ko
gwauruwa, kuma kada ka zub da jini marar laifi a wannan wuri. 4 Gama in ka lura

[*] 21:2 Da Ibraniyanci Nebukadrezzar, wanda Nebukadnezzar ne wani suna; a nan da kuma sau da dama a Irmiya da Ezekiyel. [†] 21:4 Ko kuwa Kaldiyawa; haka ma a aya 9

da bin waɗannan umarnai, to, sarakunan da suke zaune a gadon sarautar Dawuda za
su shiga ta ƙofofin wannan fada, suna hawan kekunan yaƙi da dawakai, fadawansu
da mutanensu suna musu rakiya. 5 Amma in ba ku kiyaye waɗannan umarnai ba, in
ji UBANGIJI, na rantse da kaina cewa wannan fada za tă zama kufai.' "

6 Gama ga abin da UBANGIJI yana cewa game da wannan fadar sarkin Yahuda,
"Ko da yake kina kamar Gileyad a gare ni,
kamar ƙwanƙolin Lebanon,
tabbatacce zan maishe ki hamada,
kamar garuruwan da ba mazauna.
7 Zan aika da mai hallakarwa a kanki,
kowane mutum da makamansa,
za su kuma yayyanka gumaguman al'ul na ki masu kyau
su jefa su cikin wuta.

8 "Mutane daga al'ummai da yawa za su ratsa cikin wannan birni su kuma tambayi
juna suna cewa, 'Me ya sa UBANGIJI ya yi haka da wannan babban birni?' 9 Amsar
kuwa za tă zama, 'Domin sun keta alkawarin UBANGIJI Allahnsu, suka yi sujada suka
kuma bauta wa waɗansu alloli.' "
10 Kada ku yi kuka domin sarkin da ya mutu ko ku yi makoki saboda rashinsa;
a maimako, ku yi kuka mai zafi saboda wanda aka kai zaman bauta,
domin ba zai ƙara dawowa ba
ko ya ƙara ganin ƙasarsa ta haihuwa.

11 Gama ga abin da UBANGIJI yana cewa game da Shallum* ɗan Yosiya, wanda ya
gāji mahaifinsa a matsayin sarkin Yahuda amma bai bar wurin nan ba, "Ba zai ƙara
dawowa ba. 12 Zai mutu a inda suka kai shi zaman bauta; ba zai ƙara ganin wannan
ƙasa ba."
13 "Kaiton wanda ya gina gidansa ta hanyar rashin adalci,
ɗakunansa na sama kuma ta hanyar rashin gaskiya,
yana sa mutanen ƙasarsa suna aiki a banza
ba ya biyansu wahalarsu.
14 Yana cewa, 'Zan gina wa kaina babban fada
da manyan ɗakuna.'
Ta haka sai ya yi musu manyan tagogi
ya manne musu al'ul
ya yi musu ado kuma da ruwan ja.

15 "Wannan zai mai da kai sarki ne
in kana da al'ul a kai a kai?
Mahaifinka bai kasance da abinci da abin sha ba?
Ya yi abin da yake gaskiya da kuma daidai
saboda haka kome ya kasance da lafiya da shi.
16 Ya kāre muradin matalauta da mabukata,
ta haka kome ya tafi masa daidai.
Ba abin da ake nufi da ba san ni ke nan ba?"
In ji UBANGIJI.
17 "Amma idanunka da zuciyarka
sun kahu kawai a kan ƙazamar riba,
da a kan zub da jinin marar laifi
da kuma a kan danniya da zalunci."
18 Saboda haka ga abin da UBANGIJI yana cewa game da Yehohiyakim ɗan Yosiya
sarkin Yahuda,
"Ba za su yi kuka dominsa ba,

* **22:11** A kan kuma kira shi Yehoyahaz

‘Kaito, ɗan’uwana! Kaito, ’yar’uwata!’
Ba za su yi kuka dominsa ba,
‘Kaito, maigidana! Kaito, darajarsa!’
19 Za a binne shi kamar jaki
za a ja shi a ƙasa a jefar
a bayan ƙofofin Urushalima.”

20 “Ka haura zuwa Lebanon ka yi kuka,
bari a ji muryarka a Bashan,
yi kuka daga Abarim,
gama an murƙushe dukan abokanka.
21 Na ja maka kunne sa’ad da kake zama lafiya,
amma sai ka ce, ‘Ba zan saurara ba!’
Wannan halinka ne tun kana matashi;
ba ka yi mini biyayya ba.
22 Iska za tă koro dukan makiyayanka
abokanka kuma za su tafi zaman bauta.
Sa’an nan za ka sha kunya a kuma walaƙanta ka
saboda dukan muguntarka.
23 Kai da kake zama a ‘Lebanon,’†
kai da kake sheƙa a gine-ginen al’ul
za ka yi nishi sa’ad da zafi ya auka maka,
zafi kamar na mace mai naƙuda!
24 “Muddin ina raye,” in ji Ubangiji, “ko kai, Yehohiyacin‡ ɗan Yehohiyakim sarkin
Yahuda, ka zama zoben hatimin dama a hannuna na dama, zan kwaɓe ka. 25 Zan
ba da kai ga waɗanda suke neman ranka, waɗanda kake tsoro, ga Nebukadnezzar
sarkin Babilon da kuma ga Babiloniyawa. 26 Zan jefar da kai da mahaifiyar da ta
haife ka zuwa wata ƙasa, inda babu ɗayanku da aka haifa a wurin, a can kuma za
ka mutu. 27 Ba za ka ƙara dawo ƙasar da kake marmarin dawowa ba.”
28 Wannan mutum Yehohiyacin ne da aka rena, fasasshen tukunya,
abin da babu wanda yake so?
Me ya sa za a jefar da shi da ’ya’yansa
a jefar da su a ƙasar da ba su sani ba?
29 Ya ke ƙasa, ƙasa, ƙasa,
ki ji maganar Ubangiji!
30 Ga abin da Ubangiji yana cewa,
“Ka rabu da wannan mutum sai ka ce marar ’ya’ya,
mutumin da ba zai yi nasara a rayuwarsa ba,
gama babu zuriyarsa da za tă yi nasara
babu wani da zai zauna a kursiyin Dawuda
ko ya ƙara yin mulkin Yahuda.”

# 23

### *Reshen adalci*

1 “Kaiton makiyayan da suka hallakar suka kuma warwatsar da tumakin
makiyayanta!” In ji Ubangiji. 2 Saboda haka ga abin da Ubangiji, Allah na Isra’ila
yana ce wa makiyayan da suke lura da mutanena, “Domin kun watsar da garkena
kuka kuma kore su ba ku kuma lura da su ba, zan kawo hukunci a kanku saboda
muguntar da kuka yi,” in ji Ubangiji. 3 “Ni kaina zan tattara raguwar garkena daga

† **22:23** Wato, fada a cikin Urushalima (duba 1Sar 7.2) ‡ **22:24** Da Ibraniyanci Koniya, wani suna na Yehohiyacin; haka ma a 28.

ƙasashen da na kore su zuwa zan kuma dawo da su ga makiyayansu, inda za su yi
ta haihuwa su riɓaɓɓanya. 4 Zan sa makiyaya a kansu waɗanda za su lura da su, ba
za su ƙara jin tsoro ko razana ba, ba kuwa waninsu da zai ɓace," in ji UBANGIJI.
5 "Kwanaki suna zuwa," in ji UBANGIJI,
"sa'ad da zan tā da wa Dawuda* Reshen adalci,
Sarki wanda zai yi mulki da hikima
ya kuma yi abin da yake gaskiya da kuma daidai a ƙasar.
6 A cikin zamaninsa za a ceci Yahuda
Isra'ila kuma zai zauna lafiya.
Sunan da za a kira shi ke nan,
UBANGIJI Adalcinmu.

7 "Saboda haka fa, kwanaki suna zuwa," in ji UBANGIJI, "sa'ad da mutanen ba za su
ƙara cewa, 'Muddin UBANGIJI yana raye, wanda ya fito da Isra'ila daga Masar ba,'
8 amma za su ce, 'Muddin UBANGIJI yana raye, wanda ya fito da zuriyar Isra'ila daga
ƙasar arewa da kuma daga dukan ƙasashen da ya yashe su.' Sa'an nan za su zauna
a ƙasarsu."

### *Annabawa masu ƙarya*

9 Game da annabawa kuwa,
Zuciyata ta karai;
dukan ƙasusuwana suna kaɗuwa.
Na zama kamar wanda ya bugu,
kamar mutumin da ruwan inabi ya sha kansa,
saboda UBANGIJI
da kuma maganarsa mai tsarki.
10 Kasar ta cika da mazinata;
saboda la'ana† ƙasar ta zama kango‡
makiyaya a hamada ta bushe.
Annabawa suna bin mugayen muradu
suna kuma amfani da ƙarfinsu a hanyar marar kyau.

11 "Annabi da firist dukansu biyu marasa sanin Allah ne;
har ma a cikin haikalina na tarar da muguntarsu,"
in ji UBANGIJI.
12 "Saboda haka hanyarsu za tă yi santsi;
za a jefar da su cikin duhu
a can kuwa za su fāɗi.
Zan kawo musu masifa
a shekarar da za a hukunta su,"
in ji UBANGIJI.

13 "A cikin annabawan Samariya
na ga wannan abin banƙyama.
Suna annabci ta wurin Ba'al
suna ɓad da mutanena Isra'ila.
14 A cikin annabawan Urushalima kuma
na ga wani abin bantsoro.
Suna zina suna kuma rayuwar ƙarya.
Sun ƙarfafa hannuwa masu aikata mugunta,
domin kada wani ya juya daga muguntarsa.

---

* **23:5** Ko kuwa tā da daga zuriyar Dawuda † **23:10** Ko kuwa saboda waɗannan abubuwa ‡ **23:10** Ko kuwa ƙasar yana kuka

Dukansu sun yi kama da Sodom a gare ni;
mutanen Urushalima sun yi kama da Gomorra."
15 Saboda haka, ga abin da UBANGIJI Maɗaukaki yana cewa game da annabawa,
"Zan sa su ci abinci mai ɗaci
su kuma sha ruwa mai dafi,
domin daga annabawan Urushalima
rashin sani Allah ya bazu ko'ina a ƙasar."
16 Ga abin da UBANGIJI Maɗaukaki yana cewa,
"Kada ku saurari abin da annabawan suke muku annabci;
suna cika ku da sa zuciyar ƙarya.
Suna maganar wahayi daga tunaninsu,
ba daga bakin UBANGIJI ba.
17 Suna cin gaba da ce wa waɗanda suka rena ni,
'UBANGIJI ya ce za ku zauna lafiya.'
Ga duka waɗanda suke bin taurin zukatansu kuwa
sukan ce, 'Babu lahanin da zai same ku.'
18 Amma wane ne a cikinsu ya taɓa tsaya a majalisar UBANGIJI
yǎ ga ko ya ji maganarsa?
Wa ya saurari ya kuma ji maganarsa?
19 Ga shi, hadarin UBANGIJI
zai taso cikin hasala
guguwa tana kaɗawa
a kan kawunan mugaye.
20 Fushin UBANGIJI ba zai kau ba
sai ya aikata
nufin zuciyarsa.
A kwanakin masu zuwa
za ku gane sarai.
21 Ban aiki waɗannan annabawa ba,
duk da haka sun tafi da saƙonsu;
ban yi musu magana ba,
duk da haka sun yi annabci.
22 Amma da a ce sun tsaya a majalisata,
da sun yi shelar maganata ga mutanena
sun kuma juyar da su daga mugayen hanyoyinsu
da kuma daga mugayen ayyukansu.

23 "Ni ɗin Allah na kusa ne kawai,"
in ji UBANGIJI,
"ba Allah na nesa ba?
24 Akwai wanda zai iya ɓuya a lungu har da ba zan iya ganinsa ba?"
In ji Ubangiji
"Ban cika sama da ƙasa ba?"
In ji UBANGIJI.
25 "Na ji abin da annabawa suna cewa su da suke annabcin ƙarya a sunana. Suna
cewa, 'Na yi mafarki! Na yi mafarki!' 26 Har yaushe wannan zai ci gaba a cikin
zukata annabawa masu ƙarya, waɗanda suke annabcin ruɗun tunaninsu? 27 Suna
tsammanin mafarkan da suke faɗa wa juna za su sa mutane su manta da sunana,
kamar yadda kakanninsu suka manta da sunana ta wurin yin wa Ba'al sujada. 28 Bari
annabin da ya yi mafarki ya faɗa mafarkinsa, amma bari wanda yake da maganata
ya yi ta da aminci. Gama me ya haɗa ciyawa da alkama?" In ji UBANGIJI. 29 "Maganata
ba wuta ba ce," in ji UBANGIJI, "kuma kamar gudumar da kan ragargaza dutse?

30 “Saboda haka,” in ji Ubangiji, “Ina gāba da annabawan da suke satar
maganganuna daga juna. 31 I,” in ji Ubangiji, “Ina gāba da annabawan da suke
kaɗa harsunansu sa’an nan su ce, ‘Ubangiji ne ya furta.’ 32 Tabbatacce, ina gāba
da waɗannan da suke annabci mafarkan karya,” in ji Ubangiji. “Suna faɗarsu suna
ɓad da mutanena da ƙarairayinsu na rashin hankali, duk da haka ban aike su ba,
ban kuwa umarce su ba. Ba su amfani wannan mutane ba ko kaɗan,” in ji Ubangiji.
33 “Sa’ad da waɗannan mutane, ko annabi ko firist, ya tambaye ka, ‘Mece ce
maganar§Ubangiji?’ Ka ce musu, ‘Wace magana?* Zan yashe ku, in ji Ubangiji.’ 34 In
annabi ko firist ko da wani dabam ya ce, ‘Wannan ne abin da Ubangiji yake cewa,’
zan hukunta wannan mutum da kuma gidansa. 35 Ga abin da kowannenku yana cin
gaba da ce wa abokinsa ko danginsa, ‘Mece ce amsar Ubangiji?’ Ko kuwa ‘mene
ne Ubangiji ya faɗa?’ 36 Amma kada ku ƙara ambatar ‘maganar Ubangiji’ domin
kowace maganar mutum kan zama maganarsa. Ta haka kukan lalace maganar Allah
mai rai, Ubangiji Maɗaukaki, Allahnmu. 37 Ga abin da za ku ci gaba da faɗa wa
annabi, ‘Mece ce amsar Ubangiji gare ka?’ Ko kuwa ‘mene ne Ubangiji ya faɗa?’
38 Ko da yake kuna cewa, ‘Wannan ce maganar Ubangiji,’ ga abin da Ubangiji yana
cewa kuna amfani da kalmomi, ‘Wannan ce maganar Ubangiji,’ ko da yake na ce
muku kada ku ce, ‘Wannan ce maganar Ubangiji.’ 39 Saboda haka, tabbatacce zan
manta da ku in kuma jefar da ku daga gabana tare da birnin da na ba ku da kuma
kakanninku. 40 Zan kawo muku madawwamiyar kunya, kunya ta har abada wadda
ba za a taɓa manta ba.”

# 24

### *Kwanduna biyu na ’ya’yan ɓaure*

1 Bayan Nebukadnezzar ya kwashi Yekoniya* ɗan Yehohiyakim sarkin Yahuda da
fadawa, da masu sana’a da masu zane zanen Yahuda daga Urushalima zuwa Babilon
zaman bauta, Ubangiji ya nuna mini kwanduna biyu na ’ya’yan ɓaure ajiye a gaban
haikalin Ubangiji. 2 Kwando guda yana da ’ya’yan ɓaure masu kyau sosai, kamar
waɗanda suka nuna da wuri; ɗayan kwandon kuma yana da ’ya’yan ɓaure marasa
kyau, sun yi muni har ba a iya ci.
3 Sa’an nan Ubangiji ya tambaye ni ya ce, “Me ka gani, Irmiya?”
Na ce, “’Ya’yan ɓaure. Masu kyau ɗin suna da kyau sosai, amma munanan sun yi
muni har ba a iya ci.”
4 Sai maganar Ubangiji ta zo mini cewa, 5 “Ga abin da Ubangiji, Allah na Isra’ila,
yana cewa, ‘Kamar ’ya’yan ɓauren nan masu kyau, haka zan kula da mutanen
Yahuda waɗanda aka kwaso waɗanda na fisshe su daga wannan wuri zuwa ƙasar
Babiloniyawa† 6 Idanuna za su kula da su don kyautatawarsu, zan kuma komo da su
wannan ƙasa. Zan gina su ba zan rushe su ba; zan dasa su ba kuwa zan tumɓuke
su ba. 7 Zan ba su zuciya don su san ni, cewa ni ne Ubangiji. Za su zama mutanena,
zan zama Allahnsu, gama za su komo gare ni da dukan zuciyarsu.
8 “ ‘Amma kamar ’ya’yan ɓauren nan marasa kyau, waɗanda sun yi muni har ba a
iya ci,’ in ji Ubangiji, ‘haka zan yi da Zedekiya sarkin Yahuda, fadawansa da sauran
mutanen da suka tsira a Urushalima, ko suna a wannan ƙasa ko suna zama a Masar.
9 Zan mai da su abin ƙyama da masifa ga dukan mulkokin duniya, abin zargi da abin
karin magana, abin ba’a da abin la’ana a duk inda zan kore su zuwa. 10 Zan aika da
takobi, yunwa da annoba a kansu sai an hallaka su sarai daga ƙasar da na ba su da
kuma kakanninsu.’ ”

§ **23:33** Ko kuwa nawaya (dubi Seftuwajin da Bulget) * **23:33** Da Ibraniyanci; Seftuwajin da Bulget Ku ne nawayar. (Ibraniyanci na faɗar Ubangiji da nawaya sun yi kama da juna.) * **24:1** Da Ibraniyanci Yekoniya, wani suna na Yekoniya † **24:5** Ko kuwa Kaldiyawa

# 25

*Shekaru saba'in na zaman bauta*

1 Magana ta zo wa Irmiya game da dukan mutanen Yahuda a shekara ta huɗu
ta Yehohiyakim ɗan Yosiya sarkin Yahuda, wadda ta kasance shekara ta fari ta
Nebukadnezzar sarkin Babilon. 2 Saboda haka Irmiya annabi ya ce wa dukan
mutanen Yahuda da dukan mazaunan Urushalima. 3 Shekaru ashirin da uku, daga
shekara ta goma sha uku ta Yosiya ɗan Amon sarkin Yahuda har zuwa wannan rana,
maganar UBANGIJI ta zo mini na kuma yi muku magana sau da sau, amma ba ku
saurara ba.

4 Ko da yake UBANGIJI ya aika dukan bayinsa annabawa gare ku sau da sau, ba
ku saurara ba, ba ku kuma kula ba. 5 Sun ce, "Ku juye yanzu, kowannenku, daga
mugayen hanyoyinku da mugayen ayyukanku, za ku kuwa iya zauna a ƙasar da
UBANGIJI ya ba ku da kuma kakanninku har abada abadin. 6 Kada ku bi waɗansu
alloli don ku bauta ku kuma yi musu sujada; kada ku tsokane ni in yi fushi da abin
da hannuwanku suka yi. Sa'an nan ba zan kawo muku lahani ba."

7 "Amma ba ku saurare ni ba," in ji UBANGIJI, "kun tsokane ni da abin da kuka yi
da hannuwanku, kuka kuma kawo lahani wa kanku."

8 Saboda haka UBANGIJI Maɗaukaki ya ce, "Domin kun ƙi ku saurara ga maganata,
9 zan kira dukan mutanen arewa da bawana Nebukadnezzar sarkin Babilon," in ji
UBANGIJI, "zan kuma kawo su su yi gāba da wannan ƙasa da mazaunanta da kuma
gāba da dukan al'ummai da suke kewaye. Zan hallaka su sarai in kuma mai da su abin
bantsoro da abin dariya, za su kuma zama kufai har abada. 10 Zan kawar da muryoyin
farin ciki da murna daga gare su, muryoyin amarya da na ango, ƙarar dutsen niƙa da
hasken fitila. 11 Dukan wannan ƙasa za tă zama kango, kuma waɗannan al'ummai
za su bauta wa sarkin Babilon shekaru saba'in.

12 "Amma sa'ad da shekaru saba'in ɗin suka cika, zan hukunta sarkin Babilon da
kuma al'ummarsa, ƙasar Babiloniyawa, saboda laifinsu," in ji UBANGIJI, "in kuma mai
da ita kango har abada. 13 Zan kawo wa wannan ƙasa dukan abubuwan na yi magana
a kanta, dukan abubuwan da aka rubuta a wannan littafi, abubuwan da Irmiya kuma
ya yi annabci a kan dukan al'ummai. 14 Su kansu al'ummai da sarakuna masu yawa
za su bautar da su; zan sāka musu bisa ga ayyukansu da aikin hannuwansu."

15 Ga abin da UBANGIJI, Allah na Isra'ila, ya faɗa mini, "Ka karɓi kwaf ruwan inabin
nan na fushina a wurina, ka sa dukan al'umman da na aike ka gare su, su sha.
16 Sa'ad da suka sha, za su yi ta tangaɗi su kuma yi hauka saboda takobin da zan
aika a cikinsu." 17 Saboda haka na karɓi kwaf daga hannun UBANGIJI na sa dukan
al'ummai waɗanda ya aiko ni wurinsu su sha.

18 Urushalima da garuruwan Yahuda, sarakunan da fadawanta, don su mai da su
kufai da kuma abin bantsoro da ba'a da la'ana, yadda suke a yau;
19 Fir'auna sarkin Masar, ma'aikatansa, fadawansa da dukan mutanensa, 20 da
dukan baƙin da suke can;
dukan sarakunan Uz;
dukan sarakunan Filistiyawa (waɗannan na Ashkelon, Gaza, Ekron da mutanen da
aka bari a Ashdod);
21 Edom, Mowab da Ammon;
22 dukan sarakunan Taya da Sidon;
sarakunan bakin teku a ƙetaren teku;
23 Dedan, Tema, Buz da dukan waɗanda suke a manisantan wurare;
24 dukan sarakunan Arabiya da dukan sarakunan baƙin da suke zama a hamada;
25 dukan sarakunan Zimri, Elam da Mediya;

26 da kuma dukan sarakunan arewa, nesa da kuma kusa, bi da bi, dukan mulkokin
duniya.
Bayan dukansu kuma, sai sarkin Sheshak ma yǎ sha.

27 “Sa’an nan na faɗa musu cewa, ‘Ga abin da UBANGIJI Maɗaukaki, Allah na Isra’ila,
yana cewa ku sha, ku bugu ku kuma yi amai, ku fāɗi, kada kuma ku ƙara tashi saboda
takobin da zan aiko muku.’ 28 Amma in suka ki su karɓi kwaf ɗin daga hannunka
su sha, ka faɗa musu cewa, ‘Ga abin da UBANGIJI Maɗaukaki yana cewa dole ku sha!
29 Ga shi, na sa masifa tǎ yi aiki cikin birnin da ake kira da sunana, kuna gani za ku
tafi ba hukunci? Ba za ku tafi ba hukunci ba, gama ina kawo wa dukan mazaunan
duniya takobi, in ji UBANGIJI Maɗaukaki.’
30 “Yanzu ka yi annabcin dukan waɗannan maganganu a kansu ka kuma ce musu,
“ ‘UBANGIJI zai yi ruri daga bisa;
zai yi tsawa daga mazauninsa mai tsarki
ya kuma yi ruri da ƙarfi a kan ƙasarsa.
Zai yi ihu kamar waɗanda suke matsin ’ya’yan inabi,
yi ihu a kan dukan waɗanda suke zaune a duniya.
31 Hayaniya za tǎ taso har iyakar duniya,
gama UBANGIJI zai kawo tuhume-tuhume a kan al’ummai;
zai kawo shari’a a kan dukan ’yan adam
ya kuma kashe mugaye da takobi,’ ”
in ji UBANGIJI.
32 Ga abin da UBANGIJI Maɗaukaki yana cewa,
“Duba! Masifa tana yaɗuwa
daga al’umma zuwa al’umma;
hadari mai girma yana tasowa
daga iyakar duniya.”
33 A lokacin waɗanda UBANGIJI ya kashe za su kasance a ko’ina, daga wannan bangon
duniya zuwa wancan. Ba za a yi kuka dominsu, ba za a tattara su don a binne ba,
amma za su zama kamar juji da an tsiba a ƙasa.
34 Ku yi kuka ku kuma yi makoki, ku makiyaya;
ku yi ta birgima a ƙura, ku shugabannin garke.
Gama lokacin da za a yanka ku ya zo;
za ku fāɗi ku kuma farfasa kamar tukunyar yumɓu mai kyau.
35 Makiyaya ba za su sami wurin da za su gudu su tafi ba,
shugabannin garke ba za su sami wurin kuɓuta ba.
36 Ji kukan makiyaya,
kururuwan shugabannin garke,
gama UBANGIJI yana hallaka wurin kiwo.
37 Rafi mai gudu a hankali zai zama kango
saboda zafin fushin UBANGIJI.
38 Kamar zaki zai bar wurin ɓuyarsa,
ƙasarsu kuma za tǎ zama kufai
saboda takobin masu danniya
da kuma saboda zafin fushin UBANGIJI.

# 26

*An yi wa Irmiya barazanar mutuwa*
*(Irmiya 7.1-15)*

[1] A farkon sarautar Yehohiyakim ɗan Yosiya sarkin Yahuda, wannan magana ta zo
daga wurin UBANGIJI, [2] "Ga abin da UBANGIJI yana cewa, ka tsaya a filin gidan UBANGIJI
ka kuma yi magana ga dukan mutanen garuruwan Yahuda waɗanda suka zo sujada
a gidan UBANGIJI. Ka faɗa musu kome da na umarce ka; kada ka bar wata magana.
[3] Watakila su saurara kowanne kuma ya juyo daga mugun hanyarsa. Sa'an nan in
yi juyayi in kuma janye masifar da nake shirin kawo a kansu saboda muguntar da
suka aikata. [4] Ka faɗa musu, 'Ga abin da UBANGIJI yana cewa, in ba ku saurare ni,
ku kuma bi dokata, wadda na sa a gabanku ba, [5] in kuma ba ku saurari maganganun
bayina annabawa, waɗanda na aika muku sau da sau ba (ko da yake ba ku saurara
ba), [6] to, sai in mai da gidan nan kamar Shilo, birnin nan kuma abin la'ana a cikin
al'umman duniya.' "

[7] Firistoci, annabawa da dukan mutane suka ji Irmiya yana waɗannan maganganu
a gidan UBANGIJI. [8] Amma da Irmiya ya gama faɗar wa dukan mutanen abin da
UBANGIJI ya umarce shi ya faɗa, sai firistoci, annabawa da dukan mutane suka kama
shi suka ce, "Mutuwa za ka yi! [9] Me ya sa ka yi annabci da sunan UBANGIJI cewa
wannan gida zai zama kamar Shilo, wannan birni kuma zai zama kango da hamada?"
Sai duk mutane suka tattaru kewaye da Irmiya a cikin gidan UBANGIJI.

[10] Da fadawan Yahuda suka ji haka, sai suka haura daga fada zuwa gidan UBANGIJI
suka zazzauna a wuraren zamansu a mashigin Sabuwar Kofar gidan UBANGIJI.
[11] Sa'an nan firistoci da annabawa suka ce wa fadawan da dukan mutane, "Mutumin
nan ya cancanci hukuncin kisa gama ya yi annabci gāba da wannan birni. Ku kun ji
da kunnuwanku!"

[12] Sai Irmiya ya ce wa dukan fadawa da kuma dukan mutane, "UBANGIJI ya aiko ni
in yi annabci gāba da wannan gida da wannan birni dukan abin da na faɗa. [13] Yanzu
sai ku gyara hanyoyinku da kuma ayyukanku ku yi biyayya da UBANGIJI Allahnku.
Sa'an nan UBANGIJI zai yi juyayi ya kuma janye masifar da ya furta zai kawo a kanku.
[14] Game da ni dai, ina a hannuwanku; ku yi duk abin da kuka ga ya yi kyau, ya
kuma dace a gare ku. [15] Ku tabbata dai, cewa in kuka kashe ni, za ku jawo wa kanku
alhakin jini marar laifi a kanku da a kan birnin nan da kuma a kan masu zama a
cikinsa, gama a gaskiya UBANGIJI ne ya aiko ni wurinku domin in faɗa muku dukan
maganan nan a kunnuwanku."

[16] Sai fadawa da dukan mutane suka ce wa firistoci da annabawa. "Wannan
mutum bai yi abin da ya isa hukuncin kisa ba, gama ya yi magana da sunan UBANGIJI
Allahnmu."

[17] Waɗansu daga cikin dattawan ƙasar suka zo gaba suka ce wa dukan taron jama'a,
[18] "Mika mutumin Moreshet, ya yi annabci a kwanakin Hezekiya sarkin Yahuda. Ya
ce wa dukan mutanen Yahuda, 'Ga abin da UBANGIJI Maɗaukaki yana cewa,

" 'Za a nome Sihiyona kamar gona,
Urushalima kuwa za tă zama tsibin juji,
ƙwanƙolin dutsen haikali kuwa zai zama kurmi.'*

[19] "Hezekiya sarkin Yahuda ko kuwa wani a Yahuda ya kashe shi? Ashe, Hezekiya
bai ji tsoron UBANGIJI ya nemi tagomashinsa ba? UBANGIJI kuwa bai yi juyayi ya
kuma janye masifar da ya furta zai kawo a kansu ba? Muna gab da jawo wa kanmu
muguwar masifa!"

[20] (To, fa, Uriya ɗan Shemahiya daga Kiriyat Yeyarim wani mutum ne wanda ya yi
annabci da sunan UBANGIJI; ya yi annabci irin abu ɗaya gāba da wannan birni da
wannan ƙasa yadda Irmiya ya yi. [21] Da sarki Yehohiyakim da dukan fadawansa da
ma'aikatansa suka ji wannan magana, sai sarki ya nemi a kashe shi. Amma Uriya
ya ji wannan shiri sai ya gudu zuwa Masar don tsoro. [22] Sarki Yehohiyakim ya aiki

* **26:18** Mik 3.12

Elnatan ɗan Akbor zuwa Masar, tare da waɗansu mutane. 23 Suka dawo da Uriya
daga Masar suka kawo shi wurin Sarki Yehohiyakim, wanda ya kashe shi da takobi aka kuma jefar da gawarsa a makabartar talakawa.)
24 Bugu da ƙari, Ahikam ɗan Shafan ya goyi bayan Irmiya, saboda haka ba a ba da shi ga mutane don su kashe shi ba.

# 27

*Yahuda ya bauta wa Nebukadnezzar*

1 A farkon sarautar Zedekiya ɗan Yosiya sarkin Yahuda, wannan magana ta zo wa
Irmiya daga UBANGIJI. 2 Ga abin da UBANGIJI ya ce mini, "Ka yi karkiyar itace da
maɗaurai ka ɗaura a wuyanka. 3 Sa'an nan ka aika da saƙo zuwa wurin sarakunan
Edom, Mowab, Ammon, Taya da Sidon ta bakin jakadu waɗanda suka zo Urushalima
wurin Zedekiya sarkin Yahuda. 4 Ka ba su saƙo wa iyayengijinsu su ce, 'Ga abin da
UBANGIJI Maɗaukaki, Allah na Isra'ila, yana cewa, "Ku faɗa wa iyayengijinku wannan.
5 Da ikon mai ƙarfi da kuma hannuna da na miƙa na yi duniya da mutanenta da kuma
dabbobin da suke ciki, na ba da ita ga duk wanda na ga dama. 6 Yanzu zan ba da
dukan ƙasashenku ga bawana Nebukadnezzar sarkin Babilon; zan sa namun jeji ma
su bauta masa. 7 Dukan al'ummai za su bauta masa da ɗansa da kuma jikansa har
sai har lokacin ƙasarsa ya kai; sa'an nan al'ummai masu yawa da kuma manyan sarakuna za su kasance a ƙarƙashinsa.
8 " ' "Amma fa, duk al'umma ko mulkin da bai bauta wa Nebukadnezzar sarkin Babilon ba bai kuwa rusunar da wuyarsa ga karkiyarsa ba, zan hukunta wannan al'umma da takobi, yunwa da annoba, in ji UBANGIJI, har sai na hallaka ta ta wurin
hannunsa. 9 Saboda haka kada ku saurari annabawanku, masu dubanku, masu fassarar mafarkanku, bokayenku ko masu maitancinku waɗanda suke ce muku, 'Ba
za ku bauta wa sarkin Babilon ba.' 10 Suna muku annabcin ƙaryar ne kawai da za tă
kau da ku daga ƙasarku; zan kore ku za ku kuwa hallaka. 11 Amma duk al'ummar da
ta rusuna da wuyarta a ƙarƙashin karkiyar sarkin Babilon ta kuma bauta masa, zan bar al'ummar ta zauna a ƙasarta ta noma ta, ta kuma zauna a can, in ji UBANGIJI." ' "
12 Na ba da wannan saƙo guda ga Zedekiya sarkin Yahuda. Na ce, "Ka rusunar da wuyanka a ƙarƙashin sarkin Babilon; ka bauta masa da kuma mutanensa, za ka kuwa
rayu. 13 Me ya sa kai da mutanenka za ku mutu saboda takobi, yunwa da annoba waɗanda UBANGIJI ya yi barazana wa duk al'ummar da ba za tă bauta wa sarkin
Babilon ba? 14 Kada ku saurari maganganun annabawa waɗanda suke ce muku, 'Ba
za ku bauta wa sarkin Babilon ba,' gama annabcin ƙarya suke muku. 15 'Ban aike su
ba,' in ji UBANGIJI. 'Suna annabcin ƙarya ne da sunana. Saboda haka, zan kore ku za ku kuwa hallaka, da ku da kuma annabawan da suke muku annabci.' "
16 Sai na ce wa firistoci da dukan waɗannan mutane, "Ga abin da UBANGIJI yana cewa, kada ku saurari annabawan da suke cewa, 'Ba daɗewa ba za a komo da kayan
gidan UBANGIJI daga Babilon.' Suna muku annabcin ƙarya ne. 17 Kada ku saurare su.
Ku bauta wa sarkin Babilon, za ku kuwa rayu. Don me wannan birni zai zama kufai?
18 In su annabawa ne da gaske suna kuma da maganar UBANGIJI, bari su roƙi UBANGIJI Maɗaukaki ya sa kada a kwashe kayayyakin da suka ragu a gidan UBANGIJI da kuma
a cikin fadar sarkin Yahuda da kuma cikin Urushalima a kai Babilon. 19 Gama ga
abin da UBANGIJI Maɗaukaki yana cewa game da ginshiƙai, kwatarniya, da dakalai,
da sauran kayayyaki da aka bar su a birnin nan, 20 waɗanda Nebukadnezzar sarkin
Babilon ya kwashe sa'ad da ya kame Yekoniya ɗan Yehohiyakim sarkin Yahuda zuwa zaman bauta daga Urushalima zuwa Babilon tare da dukan manyan mutanen Yahuda
da Urushalima, 21 I, ga abin da UBANGIJI Maɗaukaki, Allah na Isra'ila yana cewa game
da abubuwan da aka bari a gidan UBANGIJI da kuma a cikin fadar sarkin Yahuda da

Urushalima, 22 'Za a kwashe su zuwa Babilon a can kuwa za su kasance sai ranar
da na neme su,' in ji Ubangiji. 'Sa'an nan zan komo da su in maido da su wannan
wuri.' "

# 28

*Hananiya annabin ƙarya*

1 A wata na biyar na wannan shekara, shekara ta huɗu, a farkon sarautar
Zedekiya sarkin Yahuda, sai annabi Hananiya ɗan Azzur, wanda ya fito daga Gibeyon,
ya zo wurina a gidan Ubangiji a gaban firistoci da kuma dukan mutane, 2 "Ga
abin da Ubangiji Maɗaukaki, Allah na Isra'ila ya ce, 'Zan karya karkiyar sarkin
Babilon. 3 Cikin shekaru biyu zan komo da dukan kayayyakin gidan Ubangiji da
Nebukadnezzar sarkin Babilon ya kwashe daga wannan wuri ya kai Babilon. 4 Zan
kuma komo da Yekoniya ɗan Yehohiyakim sarkin Yahuda da kuma dukan sauran
masu zaman bauta daga Yahuda waɗanda suka tafi Babilon,' in ji Ubangiji, 'gama
zan karya karkiyar sarkin Babilon.' "

5 Sai annabi Irmiya ya amsa wa annabi Hananiya a gaban firistoci da kuma dukan
mutane waɗanda suke tsaye a gidan Ubangiji. 6 Ya ce, "Amin! Ubangiji yă sa yă zama
haka! Ubangiji yă cika maganar da ka yi annabci ta wurin komo da kayayyakin gidan
Ubangiji da kuma dukan masu zaman bauta zuwa wannan wuri daga Babilon. 7 Duk
da haka, ka saurari abin da zan faɗa a kunnenka da kuma a kunnen duka mutane,
8 Daga farko fari annabawan da suka riga ka da ni sun yi annabcin yaƙi, masifa da
annoba a kan ƙasashe masu yawa da kuma manyan mulkoki. 9 Amma annabin da
ya yi annabcin salama shi za a ɗauka a matsayin wanda Ubangiji ya aika in har abin
da ya furta ya zama gaskiya."

10 Sai annabi Hananiya ya cire karkiya daga wuyar annabi Irmiya ya karya ta,
11 ya ce a gaban dukan mutane, "Ga abin da Ubangiji yana cewa, 'A haka zan karya
karkiyar Nebukadnezzar sarkin Babilon daga wuyan dukan al'ummai a cikin shekaru
biyu.' " Da wannan, annabi Irmiya ya yi tafiyarsa.

12 Ba a daɗe ba bayan annabi Hananiya ya karya karkiya daga wuyan annabi
Irmiya, sai maganar Ubangiji ta zo wa Irmiya cewa, 13 "Je ka faɗa wa Hananiya
cewa, 'Ga abin da Ubangiji yana cewa, ka karya karkiyar katako, amma a wurinsa
za ka sami karkiyar ƙarfe. 14 Ga abin da Ubangiji Maɗaukaki, Allah na Isra'ila, yana
cewa zan sa karkiyar ƙarfe a wuyan dukan waɗannan al'ummai don in sa su bauta
wa Nebukadnezzar sarkin Babilon, za su kuwa bauta masa. Zan ma sa shi ya mallaki
namun jeji.' "

15 Sa'an nan annabi Irmiya ya ce wa annabi Hananiya, "Ka saurara, Hananiya!
Ubangiji bai aike ka ba, duk da haka ka lallashe wannan al'umma su dogara ga
ƙarya. 16 Saboda haka, ga abin da Ubangiji yana cewa, 'Ina shirin kawar da kai daga
fuskar duniya. A wannan shekara za ka mutu, domin ka yi wa'azin tawaye a kan
Ubangiji.' "

17 A wata na bakwai na wannan shekara, annabi Hananiya ya mutu.

# 29

*Wasiƙa zuwa ga masu zaman bauta*

1 Ga abin da yake cikin wasiƙar annabi Irmiya da ya aika daga Urushalima zuwa
ga sauran dattawan da suka ragu a cikin masu zaman bauta da kuma zuwa ga
firistoci, annabawa da kuma dukan sauran mutanen da Nebukadnezzar ya kwashe
zuwa zaman bauta daga Urushalima zuwa Babilon. 2 (Wannan ya faru bayan Sarki
Yekoniya da mahaifiyar sarauniya, shugabannin fada da kuma dukan shugabannin
Yahuda da Urushalima, gwanayen sana'a da masu sassaƙa suka tafi zaman bauta

daga Urushalima.) 3 Ya ba da wasiƙar ta hannun Eleyasa ɗan Shafan da Gemariya
ɗan Hilkiya, waɗanda Zedekiya sarkin Yahuda ya aika wurin Sarki Nebukadnezzar
a Babilon. Wasiƙar ta ce,

4 Ga abin da UBANGIJI Maɗaukaki, Allah na Isra'ila, yana cewa ga dukan waɗanda
aka kwashe zuwa zaman bauta daga Urushalima zuwa Babilon. 5 "Ku gina gidaje
ku zauna; ku dasa gonaki ku kuma ci abin da suka haifar. 6 Ku yi aure ku kuma haifi
'ya'ya maza da mata; ku nemi mata wa 'ya'yanku maza, ku kuma ba da 'ya'yanku
mata ga aure, saboda su ma za su haifi 'ya'ya maza da mata. Ku riɓaɓɓanya a
can, kada ku ragu. 7 Haka kuma, ku nemi zaman salama da cin gaba a birnin da
aka kai ku zaman bauta. Ku yi addu'a ga UBANGIJI saboda birnin, domin in ya ci
gaba, ku ma za ku ci gaba." 8 I, ga abin da UBANGIJI Maɗaukaki, Allah na Isra'ila
yana cewa, "Kada ku bar annabawa da masu sihiri a cikinku su ruɗe ku. Kada ku
saurari mafarkan da dā kuke ƙarfafa su su yi. 9 Suna muku annabcin ƙarya da
sunana. Ban aike su ba," in ji UBANGIJI.

10 Ga abin da UBANGIJI yana cewa, "Sa'ad da shekaru saba'in suka cika a Babilon,
zan zo muku in cika alkawarin alherina don in komo da ku zuwa wannan wuri.
11 Gama na san shirye-shiryen da na yi muku," in ji UBANGIJI, "shirye-shiryen cin
gaba ba na cutarwa ba, shirye-shiryen ba ku sa zuciya da kuma na nan gaba.
12 Sa'an nan za ku kira gare ni ku zo ku kuma yi addu'a gare ni, zan kuwa ji
ku. 13 Za ku neme ni ku kuwa same ni sa'ad da kuka neme ni da dukan zuciyarku.
14 Za ku same ni," in ji UBANGIJI, "zan kuma komo da ku daga bauta. Zan tattaro ku
daga dukan al'ummai in sa ku inda na kore ku," in ji UBANGIJI, "zan kuma komo
da ku zuwa wurin da na kwashe ku zuwa zaman bauta."

15 Za ku iya ce, "UBANGIJI ya tā da annabawa saboda mu a Babilon." 16 Amma ga
abin da UBANGIJI yana cewa game da sarki, wanda yake zaune a kursiyin Dawuda
da kuma dukan mutanen da suka ragu a wannan birni, 'yan'uwanku waɗanda
ba su tafi tare da ku zuwa zaman bauta ba. 17 I, ga abin da UBANGIJI Maɗaukaki
yana cewa, "Zan aika da takobi, yunwa da annoba a kansu zan kuma sa su zama
kamar ɓaure marar amfani da suka yi munin da ba a iya ci. 18 Zan fafare su da
takobi, yunwa da annoba zan kuma sa su zama abin ƙyama ga dukan mulkokin
duniya da kuma abin la'ana da abin bantsoro, abin dariya da abin reni, a cikin
dukan al'umman da aka kore su zuwa. 19 Gama ba su saurari maganata ba," in ji
UBANGIJI, "maganar da na aika gare su sau da sau ta bayina annabawa. Ku kuma
masu zaman bauta ba ku saurara ba," in ji UBANGIJI.

20 Saboda haka, ku ji maganar UBANGIJI, dukanku masu zaman bauta waɗanda
na aika daga Urushalima zuwa Babilon. 21 Ga abin da UBANGIJI Maɗaukaki, Allah
na Isra'ila, yana cewa game da Ahab ɗan Kolahiya da Zedekiya ɗan Ma'asehiya,
waɗanda suke muku annabcin ƙarya da sunana. "Zan ba da su ga Nebukadnezzar
sarkin Babilon, zai kuwa kashe su a gaban idanunku. 22 Saboda su, dukan masu
zaman bauta daga Yahuda waɗanda suke a Babilon za su yi amfani da wannan
la'ana cewa, 'UBANGIJI ka yi da mu kamar Zedekiya da Ahab waɗanda sarkin
Babilon ya ƙone da wuta.' 23 Gama sun aikata munanan abubuwa a Isra'ila; sun yi
zina da matan maƙwabtansu kuma da sunana suka yi ƙarya, waɗanda ban faɗa
musu su yi ba. Na san wannan kuma ni shaida ne ga haka," in ji UBANGIJI.

### *Saƙo ga Shemahiya*

24 Faɗa wa Shemahiya mutumin Nehelam, 25 "Ga abin da UBANGIJI Maɗaukaki,
Allah na Isra'ila, yana cewa ka aika da wasiƙu da sunanka ga dukan mutane a
Urushalima, zuwa ga Zefaniya ɗan Ma'asehiya firist da kuma ga sauran firistoci.
Ka ce wa Zefaniya, 26 'UBANGIJI ya naɗa ka firist a wurin Yehohiyada don ka lura da
gidan UBANGIJI; ya kamata ka sa kowane mahaukaci wanda yake yi kamar annabi

cikin turu da kuma a kangi. 27 To, me ya sa ba ka tsawata wa Irmiya daga Anatot,
wanda yana ɗauka kansa annabi a cikinku ba? 28 Ya aiko mana da saƙonsa a Babilon
cewa zai ɗauki lokaci ƙwarai. Saboda haka ku gina gidaje ku zauna; ku dasa gonaki
ku kuma ci abin da suka haifar.' "
29 Zefaniya firist kuwa, ya karanta wasiƙar annabi Irmiya. 30 Sa'an nan maganar
UBANGIJI ta zo wa Irmiya cewa, 31 "Ka aika da wannan saƙo zuwa ga dukan masu
zaman bauta cewa, 'Ga abin da UBANGIJI yana cewa game da Shemahiya, mutumin
Nehelam. Domin Shemahiya ya yi muku annabci, ko da yake ban aike shi ba, ya kuma
sa kuka gaskata ƙarya, 32 ga abin da UBANGIJI yana cewa, tabbatacce zan hukunta
Shemahiya mutumin Nehelam da zuriyarsa. Ba zai kasance da wani da ya rage a
cikin wannan mutane ba, ba kuwa zai ga abubuwa alherin da zan yi wa mutanena
ba, in ji UBANGIJI, domin ya yi wa'azin tawaye a kaina.' "

# 30

*Maidowa da Isra'ila*

1 Ga maganar da ta zo wa Irmiya daga UBANGIJI. 2 "Ga abin da UBANGIJI, Allah
na Isra'ila, yana cewa, 'Ka rubuta a cikin littafi dukan maganganun da na yi maka.
3 Kwanaki suna zuwa,' in ji UBANGIJI, 'sa'ad da zan komo da mutanena Isra'ila da
Yahuda daga bauta in kuma maido da su ga ƙasar da na ba wa kakanninsu mallaka,'
in ji UBANGIJI."
4 Ga kalmomin UBANGIJI da ya yi game da Isra'ila da Yahuda, 5 "Ga abin da UBANGIJI
yana cewa,

" 'Ana jin kukan tsoro,
razana, ba salama ba.
6 Ku tambaya ku ji.
Namiji zai iya haifi 'ya'ya?
To, me ya sa kuke ganin kowane mai ƙarfi
da hannuwansa a kwankwaso kamar mace mai naƙuda,
kowace fuska ta koma fari?
7 Kaito, gama wannan rana za tă zama mai girma!
Babu kamar ta.
Zai zama lokacin wahala wa Yaƙub,
amma za a cece shi daga cikinta.

8 " 'A wannan rana,' in ji UBANGIJI Maɗaukaki,
'Zan karya karkiya daga wuyansu
zan kuma cire musu kangi;
baƙi ba za su ƙara bautar da su ba.
9 A maimakon haka, za su bauta wa UBANGIJI Allahnsu
Dawuda sarkinsu kuwa,
wanda na tayar musu.

10 " 'Saboda haka kada ka ji tsoro, ya Yaƙub bawana;
kada ka karai, ya Isra'ila,'
in ji UBANGIJI.
'Tabbatacce zan cece ka daga wuri mai nesa,
zuriyarka daga ƙasar zaman bautansu.
Yaƙub zai sami salama da zaman lafiya,
kuma ba wanda zai sa ya ji tsoro.
11 Ina tare da kai zan kuma cece ka,'
in ji UBANGIJI.
'Ko da yake na hallakar da dukan al'umma gaba ɗaya

a inda na warwatsa ku,
ba zan hallaka ku gaba ɗaya ba.
Zan hore ku amma da adalci kaɗai;
ba zan ƙyale ku ku tafi gaba ɗaya ba hukunci ba.’
12 “Ga abin da UBANGIJI yana cewa,
“ ‘Mikinku marar warkewa ne,
raunin da kuka ji ya sha ƙarfin warkarwa.
13 Babu wanda zai yi roƙo saboda damuwarku,
ba magani domin mikinku
babu warkarwa dominku.
14 Dukan abokanku sun manta da ku;
ba su ƙara kulawa da ku.
Na buge ku kamar yadda abokin gāba zai yi
na kuma hukunta ku yadda mai mugunta zai yi,
domin laifinku da girma yake
zunubanku kuma da yawa suke.
15 Me ya sa kuke kuka a kan mikinku,
wahalarku da ba ta da magani?
Domin laifinku da girma yake da kuma zunubanku masu yawa
na yi muku waɗannan abubuwa.

16 “ ‘Amma duk wanda ya cinye ku za a cinye shi;
dukan abokan gābanku za su tafi zaman bauta.
Waɗanda suka washe ku su ma za a washe su;
dukan waɗanda suka mai da ku ganima su ma zan mai da su ganima.
17 Amma zan mayar muku da lafiya
in kuma warkar da mikinku,’ in ji UBANGIJI,
‘domin ana ce da ku yasassu,
Sihiyona wadda ba wanda ya kula da ita.’
18 “Ga abin da UBANGIJI yana cewa,
“ ‘Zan mayar da wadatar tentin Yaƙub
in kuma ji tausayin wuraren zamansa;
za a sāke gina birnin a kufansa,
fadar kuwa za tă tsaya a wurin da ya dace da ita.
19 Daga gare su waƙoƙi za su fito na godiya
da kuma sowa ta farin ciki.
Zan riɓaɓɓanya su,
ba za su kuwa ragu ba;
zan kawo musu ɗaukaka,
ba kuwa za a ƙasƙanta su ba.
20 ’Ya’yansu za su kasance kamar a kwanakin dā
jama’arsu kuma za su kahu a gabana;
zan hukunta duk wanda ya zalunce su.
21 Shugabansu zai zama ɗaya daga cikinsu;
mai mulkinsu zai taso daga cikinsu.
Zan kawo shi kusa zai kuma zo kusa da ni,
gama wane ne zai miƙa kansa
don yă yi kusa da ni?’
In ji UBANGIJI.
22 ‘Saboda haka za ku zama mutanena,
ni kuwa in zama Allahnku.’ ”

23 Ga shi, hadarin UBANGIJI
zai fasu cikin hasala,
iskar guguwa mai hurawa
a kan kawunan mugaye.
24 Fushi mai zafi na UBANGIJI ba zai kawu ba
sai ya cika
manufofin zuciyarsa gaba ɗaya.
A kwanaki masu zuwa
za ku gane wannan.

# 31

1 “A lokacin nan, zan zama Allah na dukan kabilan Isra’ila, za su kuma zama
mutanena,” in ji UBANGIJI.
2 Ga abin da UBANGIJI yana cewa,
“Mutanen da suka tsere wa takobi
za su sami tagomashi a hamada;
zan zo don in ba da hutu ga Isra’ila.”
3 UBANGIJI ya bayyana mana a dā,* yana cewa,
“Na ƙaunace ku da madawwamiyar ƙauna;
na janye ku da ƙauna marar iyaka.
4 Zan sāke gina ki
za ki kuwa sāke ginuwa, ya Budurwar Isra’ila.
Za ki kuma ɗauki ganganki
ki fita don ki yi rawa da masu farin ciki.
5 Za ki sāke dasa gonakin inabi
a kan tussan Samariya;
manoma za su yi shuka a kansu
su kuma ji daɗin amfaninsu.
6 Za a yi ranar da matsara za su tā da murya
a kan tuddan Efraim su ce,
‘Ku zo, bari mu haura Sihiyona,
zuwa wurin UBANGIJI Allahnmu.’ ”
7 Ga abin da UBANGIJI yana cewa,
“Ku rera don farin ciki wa Yaƙub;
ku yi sowa don al’ummai da suke nesa.
Ka sa a ji yabanku, ku kuma ce,
‘Ya UBANGIJI ka ceci mutanenka,
raguwar Isra’ila.’
8 Ga shi, zan kawo su daga ƙasar arewa
in tattara su daga iyakar duniya.
A cikinsu makafi da guragu za su kasance,
mata masu ciki da matan da suke naƙuda;
jama’a mai yawan gaske za su komo.
9 Za su zo da kuka;
za su yi addu’a yayinda nake komo da su.
Zan bishe su kusa da rafuffukan ruwa
a miƙaƙƙiyar hanya inda ba za su yi tuntuɓe ba,
domin ni ne mahaifin Isra’ila,
Efraim kuma ɗan farina ne.

* **31:3** Ko kuwa UBANGIJI ya bayyana mana tun daga nesa

10 “Ku ji maganar UBANGIJI, ya al’ummai;
ku yi shelarta a gaban teku masu nesa cewa,
‘Shi wanda ya watsar da Isra’ila zai tattara su
zai kuma lura da garkensa kamar makiyayi.’
11 Gama UBANGIJI zai fanshi Yaƙub
zai cece su daga hannun waɗanda suka fi su ƙarfi.
12 Za su zo su yi sowa don farin ciki a ƙwanƙolin Sihiyona;
za su yi farin ciki cikin yalwar UBANGIJI
hatsi, sabon ruwan inabi da mai,
’ya’yan garken tumaki da na shanu.
Za su zama kamar gonar da aka yi wa banruwa,
ba za su ƙara yin baƙin ciki ba.
13 ’Yan mata za su yi rawa su kuma yi murna,
haka ma samari da tsofaffi.
Zan mai da makokinsu farin ciki;
zan ta’azantar da su in kuma sa su yi farin ciki a maimakon baƙin ciki.
14 Zan ƙosar da firistoci da yalwa,
mutanena kuma za su cika da yalwa,”
in ji UBANGIJI.
15 Ga abin da UBANGIJI yana cewa,
“An ji murya daga Rama,
makoki da kuka mai zafi,
Rahila tana kuka domin ’ya’yanta
ta kuma ƙi a ta’azantar da ita
domin ’ya’yanta ba su.”
16 Ga abin da UBANGIJI yana cewa,
“Hana muryarki kuka
da kuma idanunki hawaye,
gama za a sāka wa aikinki,”
in ji UBANGIJI.
“Za su komo daga ƙasar abokin gāba.
17 Saboda haka akwai sa zuciya domin nan gaba,”
in ji UBANGIJI.
“’Ya’yanki za su komo ƙasarsu.

18 “Tabbatacce na ji gurnanin Efraim yana cewa,
‘Ka hore ni kamar ɗan maraƙi mai ƙin ji,
na kuwa horu.
Ka mayar da ni, zan kuwa dawo,
domin kai ne UBANGIJI Allahna.
19 Bayan na kauce,
sai na tuba;
bayan na gane,
sai na sunkuyar da kaina.
Na ji kunya da ƙasƙanci
domin ina ɗauke da kunyar ƙuruciyata.’
20 Efraim ba ƙaunataccen ɗana ba ne,
ɗan da nake jin daɗinsa?
Ko da yake sau da dama ina maganar gāba a kansa,
duk da haka nakan tuna da shi.
Saboda haka zuciyata tana marmarinsa;

ina da jinƙai mai girma dominsa,"
in ji UBANGIJI.

21 "Ki kafa alamun hanya;
ki sa shaidun bishewa.
Ki lura da babbar hanya da kyau,
hanyar da kika bi.
Ki komo, ya Budurwar Isra'ila,
ki komo zuwa garuruwanki.
22 Har yaushe za ki yi ta yawo,
Ya 'ya marar aminci?
UBANGIJI zai ƙirƙiro sabon abu a duniya
mace za tă kewaye† namiji."
23 Ga abin da UBANGIJI Maɗaukaki, Allah na Isra'ila yana cewa, "Sa'ad da na
komo da su daga bauta mutane a ƙasar Yahuda da cikin garuruwanta za su sāke
yi amfani da waɗannan kalmomi. 'UBANGIJI ya albarkace ka, ya mazauni mai adalci,
ya tsarkakan dutse.' 24 Mutane za su zauna tare a Yahuda da dukan garuruwansa,
manoma da waɗanda suke yawo da garkunansu. 25 Zan wartsake waɗanda suka gaji
in kuma ƙosar da waɗanda ransu ya yi yaushi."
26 A kan wannan na farka na duba kewaye. Barcina ya yi mini daɗi.
27 "Kwanaki suna zuwa," in ji UBANGIJI, "sa'ad da zan kafa gidan Isra'ila da gidan
Yahuda da 'ya'yan mutane da na dabbobi. 28 Kamar yadda na lura da su don su
tumɓuke su kuma rusar, su lalatar, su hallaka su kuma kawo masifa, haka zan lura
da su don su gina su kuma dasa," in ji UBANGIJI. 29 "A waɗannan kwanaki mutane
ba za su ƙara ce,
" 'Ubanni suka ci 'ya'yan inabi masu tsami,
haƙoran 'ya'ya suka mutu ba.'
30 A maimako, kowa zai mutu saboda zunubinsa; duk wanda ya ci 'ya'yan inabi masu
tsami, haƙoransa ne za su mutu.
31 "Lokaci yana zuwa," in ji UBANGIJI,
"sa'ad da zan yi sabon alkawari
da gidan Isra'ila
da kuma gidan Yahuda.
32 Ba zai zama kamar alkawarin
da na yi da kakanni kakanninsu ba
sa'ad da na kama su da hannu
na bishe su daga Masar,
domin sun take alkawarina,
ko da yake na zama miji a gare su,"
in ji UBANGIJI.
33 "Ga alkawarin da zan yi da gidan Isra'ila
bayan wannan lokaci," in ji UBANGIJI.
"Zan sa dokata a tunaninsu
in kuma rubuta ta a zukatansu.
Zan zama Allahnsu,
za su kuma zama mutanena.
34 Mutum ba zai ƙara koya wa maƙwabci ba,
ko ya koya wa ɗan'uwansa cewa, 'Ka san UBANGIJI,'
domin duk za su san ni,
daga ƙaraminsu har zuwa babba,"

† 31:22 Ko kuwa za tă fita neman; ko za tă kāre

in ji UBANGIJI.
“Gama zan gafarta muguntarsu
ba zan kuwa ƙara tuna da zunubansu ba.”
35 Ga abin da UBANGIJI yana cewa,
shi da ya kafa rana
don tă yi haske a yini
shi da ya sa wata da taurari
su yi haske da dare,
shi da yake dama teku
don raƙuman ruwansa su yi ruri
UBANGIJI Maɗaukaki ne sunansa.
36 “In dai wannan kafaffiyar ƙa’ida ta daina aiki a gabana,”
in ji UBANGIJI,
“to, sai zuriyar Isra’ila ta daina
zama al’umma a gabana.”
37 Ga abin da UBANGIJI yana cewa,
“In a iya auna sammai
a kuma bincike tushen duniya a ƙarƙas
to, sai in ƙi dukan zuriyar Isra’ila ke nan
saboda dukan abin da suka yi,”
in ji UBANGIJI.
38 “Kwanaki suna zuwa,” in ji UBANGIJI, “sa’ad da za a sāke gina wannan birni
domina daga Hasumiyar Hananel zuwa Kofar Kusurwa. 39 Ma’auni zai miƙe daga
can ya nausa kai tsaye zuwa tudun Gareb sa’an nan ya juya zuwa Gowa. 40 Dukan
kwarin da ake zubar da toka da kuma gawawwaki, da dukan lambatun da suke can
har zuwa Kwarin Kidron a gabas zuwa kusurwar Kofar Doki, za su zama mai tsarki
ga UBANGIJI. Ba za a ƙara tumɓuke birnin ko a rushe shi ba.”

# 32

*Irmiya ya sayi fili*

1 Ga maganar da ta zo wa Irmiya daga UBANGIJI a shekara ta goma ta Zedekiya
sarkin Yahuda, wanda ya kasance shekara ta goma sha takwas ta Nebukadnezzar.
2 Sojojin sarkin Babilon a lokacin suna ƙawanya wa Urushalima annabi Irmiya kuwa
yana a tsare a sansanin matsara a fadar Yahuda.
3 Zedekiya sarkin Yahuda fa ya sa shi a kurkuku yana cewa, “Don me kake yin
annabci? Ka ce, ‘Ga abin da UBANGIJI yana cewa, ina gab da ba da wannan birni
ga sarkin Babilon, zai kuwa cinye ta. 4 Zedekiya sarkin Yahuda ba zai kuɓuta daga
hannuwan Babiloniyawa* ba amma tabbatacce za a ba da shi ga sarkin Babilon,
zai kuwa yi masa magana fuska da fuska ya kuma gan shi da idanunsa. 5 Zai kai
Zedekiya Babilon, inda zai zauna har sai ya magance shi, in ji UBANGIJI. In ka yi yaƙi
da Babiloniyawa, ba za ka yi nasara ba.’ ”
6 Irmiya ya ce, “Maganar UBANGIJI ta zo mini cewa, 7 Hananel ɗan Shallum
ɗan’uwan mahaifinka zai zo wurinka ya ce, ‘Saya filina a Anatot, domin a matsayinka
na dangi na kurkusa hakkinka ne kuma kai ya wajaba ka saye shi.’
8 “Sa’an nan, kamar dai yadda UBANGIJI ya faɗa, sai ga Hananel yaron ɗan’uwan
mahaifina ya zo wurina a sansanin matsara ya ce, ‘Saya filina a Anatot a yankin
Benyamin. Da yake hakkinka ne ka fanshe shi ka kuma mallake shi, ka sayo shi wa
kanka.’

* 32:4 Ko kuwa Kaldiyawa; haka ma a ayoyi 5, 24, 25, 28, 29 da 43

“Sai na gane cewa wannan maganar UBANGIJI ce; 9 saboda haka sai na saye filin a
Anatot daga hannun Hananel yaron ɗan’uwan mahaifina na kuma auna masa shekel
goma sha bakwai na azurfa. 10 Na sa hannu a takarda, na buga hatimi na liƙe, na
sami shaidu na kuwa auna shekel a ma’auni. 11 Na ɗauki takardar ciniki, takardar
da aka rubuta sharuɗan a ciki, da kuma takardar da ba a liƙe ba, 12 na kuma ba wa
Baruk ɗan Neriya, ɗan Masehiya, wannan takarda a gaban Hananel yaron ɗan’uwan
mahaifina da kuma a gaban shaidun da suka sa hannu a takardan ciniki da kuma a
gaban dukan Yahudawan da suke zaune a sansanin matsaran.
13 “A gabansu na yi wa Baruk waɗannan umarnai cewa, 14 ‘Ga abin da UBANGIJI
Maɗaukaki, Allah na Isra’ila, yana cewa ka ɗauki waɗannan takardun ciniki, wanda
aka liƙe da wanda ba a liƙe ba, ka sa su a cikin tulun yumɓu don kada su lalace.
15 Gama ga abin da UBANGIJI Maɗaukaki, Allah na Isra’ila, yana cewa za a sāke saye
gidaje, filaye da gonakin inabi a wannan ƙasa.’
16 “Bayan na ba da takardun ciniki ga Baruk ɗan Neriya, sai na yi addu’a ga UBANGIJI
na ce,
17 “A, UBANGIJI Mai Iko Duka, ka yi sammai da duniya ta wurin ikonka mai girma
da kuma hannunka mai iko. Ba abin da ya gagare ka. 18 Kakan nuna ƙauna ga
dubbai amma kakan hukunta ’ya’ya saboda laifin ubanninsu a bayansu. Ya mai
girma da kuma Allah mai iko, wanda sunansa ne UBANGIJI Maɗaukaki, 19 manufofinka
da girma suke, ayyukanka kuma masu girma ne. Idanunka suna a buɗe ga dukan
hanyoyin mutane; kakan sāka wa kowa gwargwadon halinsa yadda ya dace. 20 Ka
aikata ayyukan banmamaki da kuma al’ajabai a Masar ka kuma ci gaba da su har yă
zuwa yau, a Isra’ila da kuma a cikin dukan ’yan adam, ka kuma sami sunan da har
yanzu yake naka. 21 Ka fitar da mutanenka Isra’ila daga Masar da alamu da abubuwa
banmamaki, ta wurin hannu mai iko da kuma hannu mai ƙarfi tare da banrazana
mai girma. 22 Ka ba su wannan ƙasa da ka rantse za ka ba wa kakanni kakanninsu,
ƙasa mai zub da madara da zuma. 23 Suka shiga suka mallake ta, amma ba su yi maka
biyayya ba, ba su kuma bi dokarka ba; ba su yi abin da ka umarce su ba. Saboda
haka ka kawo masifa a kansu.

24 “Duba yadda aka gina mahaurai don a kame birni. Saboda takobi, yunwa da
annoba, za a ba da birnin ga Babiloniyawa waɗanda suka kewaye shi da yaƙi.
Abin da ka faɗa ya faru, yadda kake gani yanzu. 25 Ko da yake za a ba da birnin
ga Babiloniyawa, kai, ya UBANGIJI Mai Iko Duka, ka ce mini, ‘Saye fili da azurfa ka
kuma sa a shaida cinikin.’ ”

26 Sa’an nan maganar UBANGIJI ta zo wa Irmiya cewa, 27 “Ni ne UBANGIJI Allah na
dukan ’yan adam. Akwai wani abin da ya gagare ni? 28 Saboda haka, ga abin da
UBANGIJI yana cewa, ina gab da ba da wannan birni ga Babiloniyawa da kuma ga
Nebukadnezzar sarkin Babilon, wanda zai yaƙe ta. 29 Babiloniyawan da suke yaƙi
da wannan birni za su zo ciki su cinna masa wuta; tare da gidaje inda mutane suka
tsokane ni na yi fushi ta wurin ƙona turare a rufin ɗakuna wa Ba’al suka zub da
hadayun sha wa waɗansu alloli.
30 “Mutanen Isra’ila da na Yahuda ba abin da suka yi sai mugunta a gabana daga
ƙuruciyarsu; tabbatacce, mutanen Isra’ila ba su yi kome ba sai dai tsokane ni da
abin da hannuwansu suka yi, in ji UBANGIJI. 31 Daga ranar da aka gina ta har zuwa
yanzu, wannan birni ta tā da fushina da hasalata da dole a kawar da ita daga gabana.
32 Mutanen Isra’ila da na Yahuda sun tsokane ni ta wurin dukan muguntar da suka
aikata su, sarakunansu da fadawansu, firistocinsu da annabawa, mutanen Yahuda
da mutanen Urushalima. 33 Sun juya mini bayansu ba fuskokinsu ba; ko da yake
na koyar da su sau da sau, ba su saurara ko bi horo na ba. 34 Sun kafa gumakansu
na banƙyama a cikin haikalina wanda ake kira da sunana, sun kuwa ƙazantar da
shi. 35 Sun gina masujadai kan tudu wa Ba’al a Kwarin Ben Hinnom don su miƙa

ʼyaʼyansu maza da mata hadaya ga Molek, ko da yake ban taɓa umarce su ba, bai
kuma zo mini cewa su yi abin banƙyama irin wannan ba ta haka suka sa Yahuda ya
yi zunubi.
36 “Kana cewa game da wannan birni, ‘Ta wurin takobi, yunwa da annoba za a
ba da shi ga sarkin Babilonʼ; amma ga abin da Ubangiji, Allah na Israʼila yana cewa
37 tabbatacce zan tattara su daga dukan ƙasashen da na kore su zuwa cikin fushina
da hasalata mai girma; zan komo da su wurin nan in sa su zauna lafiya. 38 Za su
zama mutanena, ni kuwa in zama Allahnsu. 39 Zan ba su zuciya ɗaya da aiki ɗaya,
don kullum su ji tsorona domin amfaninsu da kuma amfanin ʼyaʼyansu a bayansu.
40 Zan yi madawwamin alkawari da su. Ba zan taɓa barin aikata musu alheri ba, zan
kuma iza su su ji tsorona, don kada su ƙara juya daga gare ni. 41 Zan yi farin ciki a
yin musu alheri, tabbatacce zan su dasa a wannan ƙasa da dukan zuciyata da dukan
raina.
42 “Ga abin da Ubangiji yana cewa, yadda na kawo dukan wannan masifa a kan
wannan mutane, haka zan ba su wadatar da na yi musu alkawari. 43 Za a sāke sayi
filaye a wannan ƙasa da kuka ce, ‘Kango ce, ba mutane ko dabbobi, gama an ba
da ita ga Babiloniyawa.ʼ 44 Za a sayi filaye da azurfa, a kuma sa hannu a takardan
ciniki, a liƙe a kuma shaida a yankin Benyamin, a ƙauyukan kewayen Urushalima,
a garuruwan Yahuda da kuma a garuruwan ƙasar tudu, na yammancin gindin dutse
da na Negeb, domin zan maido da wadatarsu, in ji Ubangiji.”

# 33

*Alkawarin Maidowa*

1 Yayinda Irmiya yana a tsare a sansanin matsara, sai maganar Ubangiji ta zo masa
sau na biyu cewa, 2 “Ga abin da Ubangiji yana cewa, shi da ya halicci duniya, Ubangiji
wanda ya siffanta ta ya kuma kafa ta, Ubangiji ne sunansa. 3 ‘Kira gare ni zan kuwa
amsa maka in kuma faɗa maka manyan abubuwan da ba a iya kaiwa, da ba ka sani
ba.ʼ 4 Gama ga abin da Ubangiji, Allah na Israʼila yana cewa game da gidaje a wannan
birni da fadodin Yahuda da aka rurrushe domin a yi amfani da su a kan mahaurai da
kuma takobi 5 a yaƙi da Babiloniyawa. ‘Za su cika da gawawwakin mutane waɗanda
na kashe da fushina da hasalata. Zan ɓoye fuskata wa wannan birni saboda dukan
muguntarsu.
6 “ ‘Duk da haka, zan kawo lafiya da warkarwa gare ta; zan warkar da mutanena
in kuma wadata su da salama da zama lafiya. 7 Zan komo da Yahuda da Israʼila
daga bauta zan kuma sāke gina su kamar yadda suke a dā. 8 Zan tsarkake su daga
dukan zunubin da suka yi mini zan kuma gafarta musu dukan zunubansu na yin mini
tawaye. 9 Saʼan nan birnin nan za tă sa in zama sananne, farin ciki, yabo da girma
a gaban dukan alʼummai a duniya da suka ji abubuwa masu kyau da na yi mata; za
su kuma yi mamaki su kuma yi rawan jiki saboda yalwar wadata da salamar da na
ba ta.ʼ
10 “Ga abin da Ubangiji yana cewa, ‘Kuna cewa game da wannan wuri, “Kango
ne, babu mutane ko dabbobi.” Duk da haka a cikin garuruwan Yahuda da titunan
Urushalima da aka yashe, inda ba mutane ko dabbobi, za a sāke jin 11 sowa ta farin
ciki da murna, muryoyin amarya da na ango, da muryoyin waɗanda suka kawo
hadayun salama a gidan Ubangiji suna cewa,

“ ‘ “Ku yi godiya ga Ubangiji Maɗaukaki,
gama Ubangiji mai alheri ne;
ƙaunarsa za tă dawwama har abada.”

Gama zan mayar da wadatar ƙasar kamar yadda suke a dā,ʼ in ji Ubangiji.

12 “Ga abin da UBANGIJI Maɗaukaki yana cewa, ‘A wannan wuri, kango da babu
mutane ko dabbobi, cikin dukan garuruwansa za a sāke kasance da wurin kiwo don
makiyaya su hutar da garkunansu. 13 A cikin garuruwan ƙasar tudu, garuruwan
yammancin gindin dutse da na Negeb, a yankin Benyamin, a cikin ƙauyuka kewayen
Urushalima da kuma a cikin garuruwan Yahuda, garkuna za su sāke bi a ƙarƙashin
hannun mai ƙidayawa,’ in ji UBANGIJI.

14 “ ‘Kwanaki suna zuwa,’ in ji UBANGIJI, ‘sa’ad da zan cika alkawarin alheri da na
yi wa gidan Isra’ila da kuma gidan Yahuda.

15 “ ‘A waɗannan kwanaki da kuma a wannan lokaci
zan tā da Reshe mai adalci daga zuriyar Dawuda;
zai yi abin da yake daidai da kuma gaskiya a ƙasar.
16 A kwanakin nan zan ceci Yahuda
Urushalima kuma za tă zauna lafiya.
Sunan da za a kira ta shi ne,
UBANGIJI Adalcinmu.’

17 Gama ga abin da UBANGIJI yana cewa, ‘Dawuda ba zai taɓa rasa mutumin da zai
zauna a gadon sarautar Isra’ila ba, 18 ba kuwa firistoci waɗanda suke Lawiyawa za
su rasa mutumin da zai ci gaba da tsaya a gabana don miƙa hadayun ƙonawa, ya
ƙona hadayun hatsi ya kuma miƙa sadakoki ba.’ ”

19 Sai maganar UBANGIJI ta zo wa Irmiya cewa, 20 “Ga abin da UBANGIJI yana cewa,
‘In ka tā da alkawarina na rana da kuma alkawarina na dare, har dare da rana
ba za su ƙara bayyana a ƙayyadaddun lokutansu ba, 21 to, sai a tā da alkawarina
da Dawuda bawana da alkawarina da Lawiyawan da suke firistoci masu hidima a
gabana, Dawuda kuma ba zai ƙara kasance da zuriyar da za tă yi mulki. 22 Zan sa
zuriyar Dawuda bawana da kuma Lawiyawan da suke hidima a gabana su yi yawa
kamar taurarin sararin sama da kuma yashin bakin tekun da ba a iya ƙidaya.’ ”

23 Sai maganar UBANGIJI ta zo wa Irmiya cewa, 24 “Ba ka lura ba cewa waɗannan
mutane suna cewa, ‘UBANGIJI ya ƙi masarautai* biyu da ya zaɓa’? Saboda haka suka
rena mutanena ba sa ƙara ɗaukansu a matsayin al’umma. 25 Ga abin da UBANGIJI
yana cewa, ‘In ban kafa alkawarina game da rana da kuma game da dare ba in kuma
gyara dokokin sama da duniya ba, 26 to zan ƙi zuriyar Yaƙub da na Dawuda bawana
ba zan kuma zaɓi ɗaya daga cikin ’ya’yansa maza ya yi mulki a kan zuriyar Ibrahim,
Ishaku da Yaƙub ba. Gama zan mayar da wadatarsu† in kuma yi musu jinƙai.’ ”

# 34

*Gargaɗi ga Zedekiya*

1 Yayinda Nebukadnezzar sarkin Babilon da dukan sojojinsa da kuma dukan
mulkokinsa da mutanen masarautar da yake mulki suna yaƙi da Urushalima da
dukan garuruwan da suke kewaye, sai wannan magana ta zo wa Irmiya daga wurin
UBANGIJI cewa, 2 “Ga abin da UBANGIJI, Allah na Isra’ila, yana cewa ka tafi wurin
Zedekiya sarkin Yahuda ka faɗa masa, ‘Ga abin da UBANGIJI yana cewa, ina gab da ba
da wannan birni ga sarkin Babilon, zai kuwa ƙone ta. 3 Ba za ka tsere daga hannunsa
ba amma tabbatacce za a kama ka a kuma ba da kai gare shi. Za ka ga sarkin Babilon
da idanunka, zai kuwa yi magana da kai fuska da fuska. Za ka kuwa tafi Babilon.

4 “ ‘Duk da haka ka ji alkawarin UBANGIJI, ya Zedekiya sarkin Yahuda. Ga abin
da UBANGIJI yake cewa game da kai. Ba za ka mutu ta takobi ba; 5 za ka mutu
cikin salama. Yadda mutane suka ƙuna wutar jana’iza don girmama kakanninka,
sarakunan da suka riga ka, haka za su ƙuna wuta don girmama da kuma makokinka
suna cewa, “Kaito, ya maigida!” Ni kaina na yi wannan alkawari, in ji UBANGIJI.’ ”

* **33:24** Ko kuwa iyalai † **33:26** Ko kuwa zan komo da su daga bauta

6 Sa’an nan annabi Irmiya ya faɗi dukan wannan wa Zedekiya sarkin Yahuda, a
Urushalima, 7 yayinda sojojin sarkin Babilon suna yaƙi da Urushalima da sauran
garuruwan Yahuda waɗanda suka ragu, Lakish da Azeka. Waɗannan su ne birane
masu katanga kaɗai a Yahuda.
8 Maganar ta zo wa Irmiya daga Ubangiji bayan Sarki Zedekiya ya yi yarjejjeniya da
duka mutane a Urushalima ya yi shelar ’yanci wa bayi. 9 Kowa ya ’yantar da bayinsa
da suke Ibraniyawa, maza da mata; kada kowa ya riƙe bawa wanda yake mutumin
Yahuda. 10 Saboda haka dukan fadawa da mutane suka yi yarjejjeniyar cewa za su
’yantar da bayinsu maza da mata ba za su kuwa ƙara riƙe su bayi ba. Suka yarda,
suka kuma sake su. 11 Amma daga baya suka canja ra’ayoyinsu suka maido bayinsu
suka kuma sāke bautar da su.
12 Sai maganar Ubangiji ta zo wa Irmiya cewa, 13 “Ga abin da Ubangiji, Allah na
Isra’ila, yana cewa na yi alkawari da kakanni-kakanninku sa’ad da na fitar da su daga
Masar, daga ƙasar bauta. Na ce, 14 ‘A kowace shekara ta bakwai dole kowannenku yǎ
’yantar da duk wani ɗan’uwa mutumin Ibraniyawa wanda aka sayar masa. Bayan ya
yi muku hidima shekaru shida, dole ku bar shi yǎ tafi ’yantacce.’* Amma kakanninku
ba su saurare ni ba, ba su ji ni ba. 15 Bai daɗe ba da kuka tuba, kuka kuma yi abin da
yake mai kyau a idona. Kowannenku ya yi shelar ’yanci ga ɗan’uwansa. Kun ma yi
yarjejjeniya a gabana a gidan da ake kira da Sunana. 16 Amma yanzu kun juya kun
kuma ɓata sunana; kowannenku ya mayar da bayi maza da matan da kuka ’yantar
su tafi inda suka ga dama. Kun sāke tilasta su su zama bayinku.
17 “Saboda haka, ga abin da Ubangiji yana cewa, kun yi mini rashin biyayya; ba ku
yi shelar ’yanci don ’yan’uwanku ba. Saboda haka yanzu na yi muku shelar ’yanci
in ji Ubangiji, ’yanci ga mutuwa ta takobi, annoba da kuma yunwa. Zan sa ku zama
abin ƙyama ga sauran mulkokin duniya. 18 Mutanen da suka keta alkawarina da ba
su cika sharuɗan alkawarin da suka yi a gabana ba, zan yi da su kamar ɗan maraƙin
da suka yanka biyu suka bi ta tsakiyarsa. 19 Shugabannin Yahuda da Urushalima,
fadawa, firistoci da kuma dukan mutanen ƙasar waɗanda suka bi tsakanin ɗan
maraƙin da aka yanka, 20 zan ba da su ga abokan gābansu waɗanda suke neman
ransu. Gawawwakinsu za su zama abincin tsuntsayen sararin sama da na namun
jeji.
21 “Zan ba da Zedekiya sarkin Yahuda da fadawansa ga abokan gābansu waɗanda
suke neman ransu, ga sojojin sarkin Babilon, waɗanda suke janye daga gare ku.
22 Zan yi umarni, in ji Ubangiji, zan kuma komo da su wannan birni. Za su kuwa yi
yaƙi da ita, su ƙwace ta su kuma ƙone ta. Zan kuma mai da garuruwan Yahuda kufai
don kada wani ya zauna a can.”

# 35

*Mutanen Rekab*

1 Ga maganar da ta zo wa Irmiya daga wurin Ubangiji a lokacin mulkin
Yehohiyakim ɗan Yosiya sarkin Yahuda. 2 “Ka tafi wurin iyalin Rekabawa ka gayyace
su su zo a ɗaya daga cikin ɗakunan da suke gefe a gidan Ubangiji ka kuma ba su
ruwan inabi su sha.”
3 Sai na tafi don in kawo Ya’azaniya ɗan Irmiya, ɗan Habazziniya, da ’yan’uwansa
da kuma dukan ’ya’yansa maza, dukan iyalin Rekabawa. 4 Na kawo su cikin gidan
Ubangiji, a cikin ɗakin ’ya’yan Hanan ɗan Igdaliya maza mutumin Allah. Ɗakin
ne kusa da ɗakin fadawa, wanda yake bisa na Ma’asehiya ɗan Shallum mai tsaron
ƙofa. 5 Sai na ajiye ƙwarya cike da ruwan inabi da waɗansu kwaf a gaban iyalin
Rekabawan na kuma ce musu, “Ku sha ruwan inabin.”

* **34:14** M Sh 15.12

6 Amma sai suka amsa suka ce, “Ba ma shan ruwan inabi, domin kakanmu
Yehonadab ɗan Rekab ya umarce mu cewa, ‘Ko ku, ko zuriyarku kada ku sha ruwan
inabi. 7 Haka kuma ba za ku gina gidaje, ku dasa iri ko ku nome gonakin inabi ba;
kada ku kasance da wani daga cikin waɗannan abubuwa, amma dole kullum ku
zauna a tentuna. Ta haka za ku yi dogon rai a cikin ƙasar baƙuncinku.’ 8 Mun
yi biyayya da kome da kakanmu Yehonadab ɗan Rekab ya umarce mu. Mu ko
matanmu ko ’ya’yanmu maza da mata ba mu taɓa shan ruwan inabi ba 9 ba mu
kuma gina gidaje mu zauna a ciki ba ko mu yi gonakin inabi, gonaki ko hatsi ba.
10 Mun yi rayuwarmu a cikin tentuna mun kuma yi biyayya ƙwarai da kowane abin
da kakanmu Yehonadab ya umarce mu. 11 Amma da Nebukadnezzar sarkin Babilon
ya kawo wa ƙasan nan hari, sai muka ce, ‘Ku zo, dole mu tafi Urushalima don
mu tsira daga Babiloniyawa da kuma sojojin Arameyawa.’ Saboda haka ne muke
a Urushalima.”

12 Sai maganar Ubangiji ta zo wa Irmiya cewa, 13 “Ga abin da Ubangiji, Maɗaukaki,
Allah na Isra’ila, yana cewa ka tafi ka faɗa wa mutanen Yahuda da kuma mutanen
Urushalima cewa, ‘Ba za ku koyi darasi ku kuma yi biyayya da maganata ba?’ In ji
Ubangiji. 14 ‘Yehonadab ɗan Rekab ya umarci ’ya’yansa maza kada su sha ruwan
inabi sun kuma kiyaye wannan umarni. Har yă zuwa yau ba sa shan ruwan inabi,
domin sun yi biyayya da umarnin kakansu. Amma na yi muku magana sau da sau,
duk da haka ba ku yi biyayya ba. 15 Sau da sau na aika dukan bayina annabawa gare
ku. Suka ce, “Kowannenku ya juyo daga mugayen hanyoyinsa ya sabunta ayyukansa;
kada yă bi waɗansu alloli don yă bauta musu. Ta haka za ku zauna a cikin ƙasar
da na ba ku da kuma kakanninku.” Amma ba ku saurara ba, ba ku kuwa ji ni ba.
16 Zuriyar Yehonadab ɗan Rekab sun yi biyayya da umarnin da kakansu ya ba su,
amma waɗannan mutane ba su yi mini biyayya ba.’

17 “Saboda haka, ga abin da Ubangiji Allah Maɗaukaki, Allah na Isra’ila, yana
cewa, ‘Ku saurara! Zan kawo wa Yahuda da kuma kowane mutumin da yake zama
a Urushalima kowace masifar da na ambata a kansu. Na yi musu magana, amma ba
su saurara ba; na kira su, amma ba su amsa ba.’ ”

18 Sai Irmiya ya ce wa iyalin Rekabawa, “Ga abin da Ubangiji Maɗaukaki, Allah
na Isra’ila, yana cewa, ‘Kun yi biyayya da umarnin kakanku Yehonadab kuka kuma
kiyaye dukan umarnansa kuka yi kome bisa ga tsari.’ 19 Saboda haka, ga abin da
Ubangiji Maɗaukaki, Allah na Isra’ila, yana cewa, ‘Yehonadab ɗan Rekab ba zai taɓa
rasa mutumin da zai yi mini hidima ba.’ ”

# 36

*Yehohiyakim ya ƙone littafin Irmiya*

1 A shekara ta huɗu ta Yehohiyakim ɗan Yosiya sarkin Yahuda, wannan magana
ta zo wa Irmiya daga wurin Ubangiji cewa, 2 “Ka ɗauki littafi ka rubuta dukan
maganganun da na yi maka game da Isra’ila, Yahuda da kuma dukan sauran
al’ummai daga lokacin da na fara maka magana a mulkin Yosiya har zuwa yanzu.
3 Wataƙila sa’ad da mutanen Yahuda suka ji game da kowace masifar da na shirya
in auka musu, kowa ya juya daga muguwar hanyarsa; sa’an nan in gafarta musu
muguntarsu da kuma zunubinsu.”

4 Saboda haka Irmiya ya kira Baruk ɗan Neriya, yayinda Irmiya yake fadar dukan
waɗannan maganganun da Ubangiji ya faɗa masa, Baruk ya rubuta su a littafin. 5 Sai
Irmiya ya ce wa Baruk, “An hana ni, ba zan tafi haikalin Ubangiji ba. 6 Saboda haka
ka tafi gidan Ubangiji a ranar azumi ka karanta wa mutane daga littafin maganar
Ubangiji da na shibta maka ka rubuta. Ka karanta su ga dukan mutanen Yahuda
waɗanda suka zo daga garuruwansu. 7 Wataƙila za su kawo kukansu a gaban

UBANGIJI, kowanne kuma ya juya daga muguwar hanyarsa, gama fushi da hasalar
da UBANGIJI ya furta a kan mutanen nan yana da girma.”
8 Sai Baruk ɗan Neriya ya yi dukan abin da annabi Irmiya ya ce ya yi; a haikalin
UBANGIJI kuwa ya karanta maganar UBANGIJI daga littafin 9 A watan tara na shekara
ta biyar ta Yehohiyakim ɗan Yosiya sarkin Yahuda, an yi shela a yi azumi a gaban
UBANGIJI ga dukan mutanen Urushalima da waɗanda suka zo daga garuruwan
Yahuda. 10 Daga ɗakin Gemariya ɗan Shafan magatakarda, wanda yake a fili na bisa
a mashigin Sabuwar Kofar haikali, Baruk ya karanta wa dukan mutane a haikalin
UBANGIJI maganar Irmiya daga littafin.
11 Sa’ad da Mikahiya ɗan Gemariya, ɗan Shafan, ya ji dukan maganar UBANGIJI
daga littafin, 12 sai ya sauka zuwa ɗakin magatakarda a fada, inda dukan fadawa
suke zaune, Elishama magatakarda, Delahiya ɗan Shemahiya, Elnatan ɗan Akbor,
Gemariya ɗan Shafan, Zedekiya ɗan Hananiya, da dukan sauran fadawa. 13 Bayan
Mikahiya ya faɗa musu kome da ya ji Baruk ya karanta wa mutane daga littafin,
14 sai dukan fadawan suka aiki Yehudi ɗan Netaniya, ɗan Shelemiya, ɗan Kushi, ya
ce wa Baruk, “Ka zo tare da littafin da ka karanta wa mutane.” Saboda haka Baruk
ɗan Neriya ya tafi wurinsu tare da littafin a hannunsa. 15 Suka ce masa, “Zauna, ka
karanta mana littafin.”
Sai Baruk ya karanta musu littafin. 16 Da suka ji dukan maganar, sai suka dubi
juna a firgice suka ce wa Baruk, “Dole mu sanar da dukan maganan nan ga sarki.”
17 Sa’an nan suka ce wa Baruk, “Faɗa mana yadda ka yi ka rubuta dukan wannan.
Irmiya ne ya yi maka shibtar ta?”
18 Baruk ya amsa ya ce, “I, shi ne ya faɗa mini dukan wannan magana, na kuwa
rubuta su a takarda.”
19 Sa’an nan fadawan suka ce wa Baruk, “Kai da Irmiya ku je ku ɓuya. Kada ku
bari wani ya san inda kuke.”
20 Bayan da suka ajiye littafin a ɗakin Elishama magatakarda, sai suka tafi wurin
sarki a fili suka sanar da shi kome. 21 Sai sarki ya aiki Yehudi ya kawo littafin daga
ɗakin Elishama magatakarda ya kuma karanta wa sarki da kuma dukan fadawan da
suke tsaye kusa da shi. 22 A watan tara ne sarki kuwa yana zaune a gidansa na rani,
wuta kuwa tana ci a kasko a gabansa. 23 Duk sa’ad da Yehudi ya karanta sashi uku
ko huɗu na littafin, sai sarkin ya sa wuƙa ya yanke su, ya zuba a wutar da take ci a
kasko, da haka ya ƙone dukan littafin. 24 Sai sarki da dukan masu yin masa hidima
waɗanda suke jin maganan nan ba su firgita ba, balle su keta rigunansu. 25 Ko da
yake Elnatan, Delahiya da Gemariya sun roƙi sarki kada yǎ ƙone littafin, bai saurare
su ba. 26 A maimakon haka, sai sarki ya umarci Yerameyel ɗan sarki, Serahiya ɗan
Azriyel da Shelemiya ɗan Abdeyel su kama Baruk marubuci da Irmiya annabi. Amma
UBANGIJI ya ɓoye su.
27 Bayan sarki ya ƙone littafin da ya ƙunshi maganar da Baruk ya rubuta daga
shibtar Irmiya, sai maganar UBANGIJI ta zo wa Irmiya cewa, 28 “Ka ɗauki wani littafi
ka rubuta a kansa dukan maganar da littafi na farin ya ƙunsa, wanda Yehohiyakim
sarkin Yahuda ya ƙone. 29 Ka kuma faɗa wa Yehohiyakim sarkin Yahuda cewa,
‘Ga abin da UBANGIJI yana cewa, ka ƙone wancan littafin ka kuma ce, “Don me ka
rubuta a cikinsa, cewa lalle sarkin Babilon zai zo ya hallaka wannan ƙasa, zai kashe
mutum duk da dabba?” 30 Saboda haka, ga abin da UBANGIJI yana cewa game da
Yehohiyakim sarkin Yahuda. Ba zai kasance da wani wanda zai zauna a kan gadon
sarautar Dawuda ba; za a jefar da gawarsa ta sha zafi da rana da dare kuma ta sha
matsanancin sanyi. 31 Zan hukunta shi da kuma ’ya’yansa da masu hidimarsa saboda
muguntarsu; zan kawo kowace masifar da na furta a kansu da kuma waɗanda suke
zama a Urushalima da na Yahuda, domin sun ƙi su saurara.’ ”

32 Sai Irmiya ta ɗauko wani littafi ya ba wa Baruk ɗan Neriya marubuci, kuma
yayinda Irmiya yake shibtawa, Baruk ya rubuta a littafin dukan maganar da take a
littafin da Yehohiyakim sarkin Yahuda ya ƙone. Ya kuma ƙara ire-iren maganganun
nan a kansu.

## 37

*Irmiya a kurkuku*

1 Nebukadnezzar sarkin Babilon ya naɗa Zedekiya ɗan Yosiya sarkin Yahuda; ya yi
mulki a madadin Yehohiyacin ɗan Yehohiyakim. 2 Shi da masu yin masa hidima da
mutanen ƙasar ba su kula da maganar da Ubangiji ya yi ta wurin Irmiya annabi ba.
3 Sai sarki Zedekiya ya aiki Yehukal ɗan Shelemiya tare da firist nan Zefaniya ɗan
Ma'asehiya da wannan saƙo cewa, "Ina roƙonka ka yi addu'a ga Ubangiji Allahnmu
saboda mu."
4 To, fa, Irmiya ya sami 'yancin kai da kawowa a cikin mutane, gama ba a riga an
sa shi a kurkuku ba. 5 Sojojin Fir'auna suka fita daga Masar, sa'ad da Babiloniyawa
waɗanda suke ƙawanya wa Urushalima suka ji labari game da su, sai suka janye
daga Urushalima.
6 Sai maganar Ubangiji ta zo wa Irmiya annabi cewa, 7 "Ga abin da Ubangiji, Allah
na Isra'ila, yana cewa ka faɗa wa sarkin Yahuda, wanda ya aika a neme ni cewa,
'Sojojin Fir'aunan da suka fito su taimake ka, za su koma ƙasarsu, Masar. 8 Sa'an
nan Babiloniyawa za su koma su yaƙi wannan birni su ci ta su kuma ƙone shi.'
9 "Ga abin da Ubangiji yana cewa, kada ku ruɗe kanku, kuna tsammani,
'Tabbatacce Babiloniyawa sun bar mu.' Ba za su bari ba! 10 Ko da a ce za ku ci
dukan sojojin Babiloniyawan da suke yaƙi da ku har raunana ne kawai aka bari a
tentunansu, za su fito su ƙone wannan birni."
11 Bayan sojojin Babiloniyawa suka janye daga Urushalima saboda sojojin Fir'auna,
12 sai Irmiya ya bar birnin don yǎ je yankin Benyamin ya sami rabon mallaka a cikin
mutane a can. 13 Amma sa'ad da ya kai Kofar Benyamin, sai hafsa mai tsaro, wanda
ake kira Iriya ɗan Shelemiya, ɗan Hananiya, ya kama shi ya kuma ce, "Kana gudu
daga Babiloniyawa ne!"
14 Sai Irmiya ya ce, "Ba gaskiya ba ce, ba na gudu daga Babiloniyawa." Amma Iriya
bai saurare shi ba; a maimako, ya kama Irmiya ya kawo shi wurin fadawa. 15 Suka
yi fushi da Irmiya suka sa aka yi masa dūka aka kuma jefa shi cikin kurkuku a gidan
Yonatan magatakarda, gama an mai da gidansa ya zama kurkuku.
16 Aka sa Irmiya a can cikin kurkuku, inda ya kasance kwanaki masu yawa. 17 Sa'an
nan Sarki Zedekiya ya aika a kawo shi aka kuma kawo shi fada, inda ya tambaye shi
a kaɗaice ya ce, "Akwai wata magana daga Ubangiji?"
Irmiya ya amsa ya ce, "I, za a ba da kai ga sarkin Babilon."
18 Sai Irmiya ya ce wa Sarki Zedekiya, "Wane laifi na yi maka ko fadawanka ko kuwa
wannan mutane, da ka sa aka jefa ni cikin kurkuku? 19 Ina annabawanka waɗanda
suka yi maka annabci suna cewa, 'Sarkin Babilon ba zai yaƙe ka ko wannan ƙasa ba'?
20 Amma yanzu, ranka yǎ daɗe, sarkina, ka saurara. Bari in kawo kukata a gabanka.
Kada ka mai da ni gidan Yonatan magatakarda, in ba haka zan mutu a can."
21 Sarki Zedekiya ya yi umarni a ajiye Irmiya a sansanin matsara a kuma ba shi
burodi daga titin masu gashin burodi kowace rana sai duka burodi a birnin ya ƙare.
Saboda haka Irmiya ya zauna a sansanin matsara.

## 38

*An jefa Irmiya a rijiya marar ruwa*

1 Shefatiya ɗan Mattan, Gedaliya ɗan Fashhur, Yukal* ɗan Shelemiya da Fashhur
ɗan Malkiya ya ji abin da Irmiya yana faɗa wa dukan mutane sa'ad da ya ce, 2 "Ga
abin da Ubangiji yana cewa, 'Duk wanda ya zauna a wannan birni zai mutu ta takobi,
yunwa ko annoba, amma duk wanda ya je wurin Babiloniyawa† zai rayu. Zai tsira
da ransa, ya rayu.' 3 Kuma ga abin da Ubangiji yana cewa, 'Tabbatacce za a ba da
wannan birni ga sojojin sarkin Babilon, wanda zai ci shi.' "
4 Sai fadawa suka ce wa sarki, "Ya kamata a kashe wannan mutum. Yana karya
zuciyar sojojin da suka ragu a birnin, da zuciyar sauran mutane, ta wurin abubuwan
da yake faɗa musu. Wannan mutum ba ya neman jin daɗin zaman wannan sai dai
wahala."
5 "Yana a hannuwanku" Sarki Zedekiya ya amsa. "Sarki ba zai iya yin kome ya
hana ku ba."
6 Saboda haka suka kama Irmiya suka sa a rijiyar da ba ruwa a ciki ta Malkiya,
ɗan sarki, wadda take a sansanin matsara. Suka saukar da Irmiya cikin rijiyar da ba
ruwa da igiya; babu ruwa a cikinta, sai laka, Irmiya ya nutse cikin laka.
7 Amma Ebed-Melek mutumin Kush,‡ wani hafsa§ a fada, ya ji cewa sun sa Irmiya
a rijiyar da ba ruwa. Yayinda sarki yana zama a Kofar Benyamin, 8 Ebed-Melek ya
fita daga fadar ya ce masa, 9 "Ranka yă daɗe sarki, waɗannan mutane sun yi mugun
abu a duk abin da suka yi wa Irmiya annabi. Sun jefa shi cikin rijiyar da ba ruwa,
inda zai mutu da yunwa gama ba sauran wani burodi a birnin."
10 Sai sarki ya umarce Ebed-Melek mutumin Kush, "Ka ɗauko mutane talatin daga
nan ku fid da Irmiya annabi daga rijiyar kafin ya mutu."
11 Saboda haka Ebed-Melek ya ɗauki mutane tare da shi suka shiga ɗaki a
ƙarƙashin baitulmali a cikin fada. Ya ɗauko waɗansu tsofaffin tsummoki da tsofaffi
riguna daga can ya kuma zurara su da igiya wa Irmiya a cikin rijiyar. 12 Ebed-Melek
mutumin Kush ya ce wa Irmiya, "Ka sa waɗannan tsummoki da tsofaffin rigunan a
hammatarka, ya zarga igiya." Irmiya ya yi haka, 13 suka kuma ja shi sama da igiya
suka fid da shi daga rijiyar. Irmiya kuwa ya zauna a sansanin matsara.

### *Zedekiya ya sāke yi wa Irmiya tambayoyi*

14 Sai Sarki Zedekiya ya aika a kawo Irmiya annabi, ya sa aka kawo shi a ƙofa ta
uku ta haikalin Ubangiji. Sai sarki ya ce wa Irmiya, "Zan tambaye ka wani abu, kada
ka ɓoye mini wani abu."
15 Irmiya ya ce wa Zedekiya, "In na ba ka amsa, ba za ka kashe ni ba? Ko da na ba
ka shawara, ba za ka saurare ni ba."
16 Amma Sarki Zedekiya ya yi wannan rantsuwa a kaɗaice ga Irmiya cewa, "Muddin
Ubangiji yana a raye, wanda ya ba mu numfashi, ba zan kashe ka ko in ba da kai ga
waɗanda suke neman ranka ba."
17 Sa'an nan Irmiya ya ce wa Zedekiya, "Ga abin da Ubangiji Allah Maɗaukaki,
Allah na Isra'ila, yana cewa, 'In ka miƙa wuya ga hafsoshin sarkin Babilon, za a
bar ka da rai ba za a kuma ƙone wannan birni ba; da kai da iyalinka za ku rayu.
18 Amma in ba ka miƙa wuya ga hafsoshin sarkin Babilon ba, za a ba da wannan
birni ga Babiloniyawa za su kuma cinna mata wuta; kai kanka ba za ka tsira daga
hannuwansu ba.' "
19 Sarki Zedekiya ya ce wa Irmiya, "Ina jin tsoron Yahudawan da suka tafi
wurin Babiloniyawa, gama Babiloniyawa mai yiwuwa su ba da ni gare su su kuma
wulaƙanta ni."
20 Irmiya ya ce, "Ba za su ba da kai ba, ka yi biyayya ga Ubangiji ta wurin yin abin
da na faɗa maka. Ta haka zai zama maka da amfani, za ka kuwa rayu. 21 Amma in

---

* **38:1** Da Ibraniyanci Yukal, wani sunan Yukal † **38:2** Ko kuwa Kaldiyawa; haka ma a ayoyi 18, 19 da 23
‡ **38:7** Mai yiwuwa daga yankin Nilu na Bisa § **38:7** Ko kuwa wani bābā

ka ƙi miƙa wuya, ga abin da UBANGIJI ya bayyana mini. 22 Za a fitar da dukan matan
da suka ragu a fadan sarkin Yahuda wa hafsoshin sarkin Babilon. Waɗannan mata
za su ce maka,
" 'Sun ruɗe ka suka kuma rinjaye ka,
waɗannan abokanka.
Kafafunka sun nutse a cikin laka;
abokanka sun yashe ka.'
23 "Za a kawo dukan matanka da 'ya'yanka wa Babiloniyawa. Kai kanka ba za ka
tsira daga hannuwansu ba amma za su sa sarkin Babilon zai kama ka; za a kuma
ƙone wannan birni.*"
24 Sai Zedekiya ya ce wa Irmiya, "Kada ka bar wani ya san wannan zance, in ba
haka ba za ka mutu. 25 In fadawa suka ji cewa na yi magana da kai, suka kuma zo
wurinka suka ce, 'Faɗa mana abin da ka faɗa wa sarki da kuma abin da sarki ya
faɗa maka; kada ka ɓoye mana, in ba haka za mu kashe ka,' 26 sai ka ce musu cewa,
'Na roƙi sarki kada yă mai da ni gidan Yonatan in mutu a can.' "
27 Dukan fadawa kuwa suka zo wurin Irmiya suka tambaye shi, ya kuma faɗa musu
dukan abin da sarki ya umarce shi ya faɗa. Saboda haka ba su ƙara ce masa kome
ba, gama ba wanda ya ji zance da suka yi da sarki.
28 Irmiya kuwa ya zauna a sansanin masu gadi har ranar da aka ci Urushalima da
yaƙi.

### *Fāɗuwar Urushalima*
*(Irmiya 52.4-16; 2 Sarakuna 25.1-12)*

Ga yadda aka ci Urushalima,

# 39

1 A shekara ta tara ta Zedekiya sarkin Yahuda, a wata na goma, Nebukadnezzar
sarkin Babilon ya fita yaƙi da Urushalima da dukan sojojinsa ya kuma yi mata
ƙawanya. 2 A rana ta tara ga watan huɗu a shekara ta goma sha ɗaya ta mulkin
Zedekiya, sai aka huda katanga. 3 Sa'an nan dukan fadawan sarkin Babilon suka shiga
suka zazzauna a Kofar Tsakiya. Wato, Nergal-Sharezer na Samgar-Nebo, Sarsekim
wani babban hafsa, Nergal-Sharezer bafade mai girma da dukan sauran fadawan
sarkin Babilon. 4 Sa'ad da Zedekiya sarkin Yahuda da dukan sojoji suka gan su, sai
suka gudu; suka bar birnin da dare ta hanyar lambun sarki, ta ƙofar da take tsakanin
katanga biyu, suka nufi waje Araba.*
5 Amma sojojin Babiloniyawa suka bi su, suka ci wa Zedekiya a filayen Yeriko. Suka
kama shi suka kai shi wurin Nebukadnezzar a Ribla a ƙasar Hamat, inda aka yanke
masa hukunci. 6 A can Ribla sarkin Babilon ya kashe 'ya'yan Zedekiya a idanunsa
aka kuma kashe dukan manyan mutanen Yahuda. 7 Sa'an nan ya ƙwaƙule idanun
Zedekiya ya kuma buga masa ƙuƙumi, ya kai shi Babilon.
8 Sai Babiloniyawa suka cinna wa fadar da kuma gidajen mutane wuta suka farfasa
katangar Urushalima. 9 Nebuzaradan shugaban matsaran sarki ya kwashi mutanen
da suka rage a birnin zuwa zaman bauta a Babilon, tare da waɗanda suka riga suka
tafi wurinsa, da kuma sauran mutanen. 10 Amma Nebuzaradan shugaban matsaran
ya bar waɗansu matalauta a ƙasar Yahuda, su da ba su da kome; a lokacin kuwa ya
ba su gonakin inabi da kuma filaye.
11 To, fa, Nebukadnezzar sarkin Babilon ya ba da wannan umarnai game da Irmiya
ta wurin Nebuzaradan shugaban matsaran sarki cewa, 12 "Ka ɗauke shi ka lura da
shi da kyau, kada ka yi masa wani mugun abu, amma ka yi masa dukan abin da yake

* **38:23** Ko kuwa za ka kuma sa wannan birni yă * **39:4** Ko kuwa Kwarin Urdun

so.” 13 Saboda haka Nebuzaradan shugaban matsara, Nebushazban babban hafsa,
Nergal-Sharezer bafade mai girma da sauran hafsoshin sarkin Babilon 14 suka aika
aka kawo Irmiya daga filin matsar. Suka miƙa shi ga Gedaliya ɗan Ahikam, ɗan
Shafan, don yă kai shi gidansa. Saboda haka ya zauna a can a cikin mutanensa.
15 Yayinda aka kulle Irmiya a sansanin matsara, maganar UBANGIJI ta zo masa cewa,
16 “Tafi ka faɗa wa Ebed-Melek mutumin Kush, ‘Ga abin da UBANGIJI Maɗaukaki, Allah
na Isra’ila, yana cewa ina gab da cika maganata a kan wannan birni ta wurin masifa,
ba wadata ba. A lokacin za tă cika a idanunka. 17 Amma zan kuɓutar da kai a wannan
rana, in ji UBANGIJI; ba zan ba da kai ga waɗanda kake tsoronsu ba. 18 Zan cece ka;
ba za ka mutu ta wurin takobi ba amma za ka tsira da ranka, domin ka dogara gare
ni, in ji UBANGIJI.’ ”

# 40

## *An ’yantar da Irmiya*

1 Sai magana ta zo wa Irmiya daga UBANGIJI bayan Nebuzaradan shugaban
matsaran sarki ya sake shi a Rama. Ya sami Irmiya a daure da sarƙoƙi a cikin sauran
kamammu daga Urushalima da kuma Yahuda waɗanda ake kaiwa zaman bauta a
Babilon. 2 Sa’ad da shugaban matsaran ya sami Irmiya sai ya ce masa, “UBANGIJI
Allahnka ya sa wannan masifa saboda wannan wuri. 3 Yanzu kuma UBANGIJI ya
cika shi; ya yi kamar yadda ya faɗa. Dukan wannan ya faru domin kun yi zunubi
ga UBANGIJI ba ku kuwa yi masa biyayya ba. 4 Amma yau ina ’yantar da kai daga
sarƙoƙin da suke a hannuwanka. Zo mu tafi Babilon, in kana so, zan kuwa lura da
kai; amma in ba ka so, kada ka zo. Ga shi, dukan ƙasar tana a gabanka; ka tafi duk
inda ka so.” 5 Amma, kafin Irmiya yă juya yă tafi,* Nebuzaradan ya ƙara da cewa,
“Ka koma wurin Gedaliya ɗan Ahikam, ɗan Shafan, wanda sarkin Babilon ya naɗa
a kan garuruwan Yahuda, ka zauna da shi a cikin mutane, ko kuwa ka tafi duk inda
ka ga dama.”

Sa’an nan shugaban ya ba shi abinci da kuma kyauta sai ya bar shi ya tafi. 6 Saboda
haka Irmiya ya tafi wurin Gedaliya ɗan Ahikam, a Mizfa ya zauna tare da shi a cikin
mutanen da aka bari a ƙasar.

## *An yi wa Gedaliya kisan gilla*

7 Sa’ad da dukan shugabannin hafsoshin tare da mutanen da suke a karkara
suka ji cewa sarkin Babilon ya naɗa Gedaliya ɗan Ahikam gwamna a kan ƙasar
ya kuma sa shi ya lura da maza, mata da ’ya’yan da suke mafi talauci a ƙasar da
waɗanda ba a kwashe zuwa zaman bauta a Babilon ba, 8 sai suka zo wurin Gedaliya
a Mizfa, Ishmayel ɗan Netaniya, Yohanan da Yonatan ’ya’yan Kareya, da Serahiya
ɗan Tanhumet maza, ’ya’yan Efai maza, mutumin Netofa, da Yezaniya† ɗan mutumin
Ma’aka da mutanensu. 9 Gedaliya ɗan Ahikam, ɗan Shafan, ya yi rantsuwa don yă
tabbatar musu da mutanensu. Ya ce, “Kada ku ji tsoron bauta wa Babiloniyawa.‡ Ku
zauna a ƙasar ku bauta wa sarkin Babilon, zai kuma yi muku amfani. 10 Ni kaina zan
zauna a Mizfa in zama wakilinku a gaban Babiloniyawa waɗanda za su zo wurinmu,
amma ku girbe ruwan inabi, ’ya’yan itatuwa na kaka, da mai, ku zuba su a tulunan
ajiyarku, ku kuma zauna a garuruwan da kuka ci.”
11 Sa’ad da dukan Yahudawan da suke a Mowab, Ammon, Edom da sauran ƙasashe
suka ji cewa sarkin Babilon ya bar raguwa a Yahuda ya kuma naɗa Gedaliya ɗan
Ahikam, ɗan Shafan gwamna a kansu, 12 sai suka dawo ƙasar Yahuda, wurin Gedaliya
a Mizfa, daga dukan ƙasashen da suke a warwatse. Suka girbe ruwan inabi a yalwace
da ’ya’yan itatuwan kaka.

---

* **40:5** Ko kuwa Irmiya ya amsa † **40:8** Da Ibraniyanci Yezaniya, wani suna na Ya’azaniya ‡ **40:9** Ko kuwa Kaldiyawa; haka ma a aya 10

13 Yohanan ɗan Kareya da dukan manyan sojoji da suke a karkara suka zo wurin
Gedaliya a Mizfa 14 suka ce masa, "Ba ka san cewa Ba'alis sarkin Ammonawa ya
aiki Ishmayel ɗan Netaniya ya ɗauke ranka ba?" Amma Gedaliya ɗan Ahikam bai
gaskata su ba.
15 Sai Yohanan ɗan Kareya ya yi wa Gedaliya a Mizfa magana a asirce ya ce, "Bari
in tafi in kashe Ishmayel ɗan Netaniya, ba kuwa wanda zai sani. Me zai sa ya ɗauke
ranka ya watsar da dukan Yahudawan da suka taru kewaye da kai har waɗanda suka
ragu na Yahuda su hallaka?"
16 Amma Gedaliya ɗan Ahikam ya ce wa Yohanan ɗan Kareya, "Kada ka yi irin
wannan abu! Abin da kake faɗa game da Ishmayel ba gaskiya ba ne."

# 41

1 A wata na goma sha bakwai sai Ishmayel ɗan Netaniya, ɗan Elishama, wanda yake
mai jinin sarauta yake kuma ɗaya daga cikin hafsoshin sarki, ya zo tare da mutum
goma wurin Gedaliya ɗan Ahikam a Mizfa. Yayinda suke ci tare a can, 2 sai Ishmayel
ɗan Netaniya da mutum goma waɗanda suke tare da shi suka kashe Gedaliya ɗan
Ahikam, ɗan Shafan, da takobi, suka kashe wannan da sarkin Babilon ya naɗa a
matsayin gwamna a kan ƙasar. 3 Ishmayel ya kuma kashe dukan Yahudawan da
suke tare da Gedaliya a Mizfa, haka ma ya yi da sojojin Babiloniyawan da suke can.
4 Kashegari bayan an kashe Gedaliya, kafin wani ya san abin da ya faru, 5 sai ga
mutane tamanin daga Shekem, Shilo da Samariya suka zo da gemunsu a aske, da
tufafinsu a kece, da jikunansu a tsage, suka kawo hadayun gari da turare tare da
su a gidan UBANGIJI. 6 Ishmayel ɗan Netaniya ya fito daga Mizfa don yǎ sadu da su.
Sa'ad da ya sadu da su, sai ya ce, "Ku zo wurin Gedaliya ɗan Ahikam." 7 Da suka
shiga cikin birni, sai Ishmayel ɗan Netaniya da mutanen da suke tare da shi suka
karkashe su suka zubar a rijiya. 8 Amma goma daga cikinsu suka ce wa Ishmayel,
"Kada ka kashe mu, muna da alkama da sha'ir, mai da kuma zuma, a ɓoye a gona."
Saboda haka ka bar mu kada ka kashe mu tare da sauran. 9 To, rijiyar da ya zubar
da gawawwakin mutanen da ya kashe tare da ta Gedaliya ita ce wadda Sarki Asa ya
haƙa a matsayin kāriya saboda Ba'asha sarkin Isra'ila. Ishmayel ɗan Netaniya ya
cika ta da gawawwaki.
10 Ishmayel ya mai da dukan sauran mutanen da suke Mizfa bayi 'ya'yan sarki mata
tare da dukan sauran da aka bari a can, waɗanda Nebuzaradan shugaban matsaran
sarki ya bari a hannun Gedaliya ɗan Ahikam. Ishmayel ɗan Netaniya ya kwashe su
ganima, ya tashi don yǎ haye zuwa wurin Ammonawa.
11 Sa'ad da Yohanan ɗan Kareya da dukan shugabannin sojojin da suke tare da
shi suka ji dukan laifofin da Ishmayel ɗan Netaniya ya aikata, 12 sai suka kwashe
dukan mutanensu suka tafi don su yaƙi Ishmayel ɗan Netaniya. Suka iske shi kusa
da babban tafki a Gibeyon. 13 Sa'ad da dukan mutanen da suke tare da Ishmayel
suka ga Yohanan ɗan Kareya da shugabannin sojojin da suke tare da shi, sai suka yi
farin ciki. 14 Dukan mutanen da Ishmayel ya kame a Mizfa suka juya, suka tafi wurin
Yohanan ɗan Kareya. 15 Amma Ishmayel ɗan Netaniya da mutanensa takwas suka
tsere daga Yohanan suka gudu zuwa wurin Ammonawa.

### *Gudu zuwa Masar*

16 Sai Yohanan ɗan Kareya da dukan shugabannin sojojin da suke tare da shi suka
bi da dukan waɗanda suka tsira daga Mizfa waɗanda ya karɓe daga Ishmayel ɗan
Netaniya bayan ya kashe Gedaliya ɗan Ahikam, wato, sojoji, mata, yara da fadawan
da ya kawo daga Gibeyon 17 Sai suka ci gaba, suka dakata a Gerut Kimham kusa
da Betlehem a kan hanyarsu zuwa Masar 18 don su kuɓuce wa Babiloniyawa. Sun ji

tsoronsu domin Ishmayel ɗan Netaniya ya kashe Gedaliya ɗan Ahikam, wanda sarkin
Babilon ya naɗa gwamna a kan ƙasar.

# 42

1 Sa'an nan dukan shugabannin sojoji, haɗe da Yohanan ɗan Kareya da Yezaniya*
ɗan Hoshahiya, da dukan mutane daga ƙarami zuwa babba, suka zo wurin 2 Irmiya
annabi suka ce masa, "Muna roƙonka ka ji kukanmu ka kuma yi addu'a ga Ubangiji
Allahnka saboda dukan wannan raguwar mutane. Gama kamar yadda kake gani
yanzu, ko da yake dā muna da yawa, yanzu ɗan kaɗan muka rage. 3 Ka yi addu'a
cewa Ubangiji Allahnka zai faɗa mana inda za mu tafi da kuma abin da za mu yi."

4 Sai Irmiya ya amsa ya ce, "Na ji ku, tabbatacce zan yi addu'a ga Ubangiji Allahnku
yadda kuka roƙa; zan faɗa muku duk abin da Ubangiji ya faɗa ba kuwa zan ɓoye
muku kome ba."

5 Sa'an nan suka ce wa Irmiya, "Ubangiji ya zama shaida na gaskiya da kuma
aminci a kanmu in ba mu yi bisa da duk abin da Ubangiji Allahnka ya aike ka ka
faɗa mana ba. 6 Ko ya gamshe mu ko bai gamshe mu ba, za mu yi biyayya da Ubangiji
Allahnmu, ga wanda muke aikan ka, saboda ya zama mana da amfani, gama za mu
yi biyayya da Ubangiji Allahnmu."

7 Bayan kwana goma sai maganar Ubangiji ta zo wa Irmiya. 8 Saboda haka ya
kira Yohanan ɗan Kareya da dukan shugabannin sojoji waɗanda suke tare da shi da
dukan jama'a daga ƙarami zuwa babba. 9 Ya ce musu, "Ga abin da Ubangiji, Allah
na Isra'ila, wanda kuka aike ni gare shi don in gabatar da kukanku, yana cewa, 10 'In
kuka zauna a wannan ƙasa, zan gina ku ba zan kuwa rushe ku ba; zan dasa ku ba
kuwa zan tumɓuke ku ba, gama ina baƙin ciki a kan masifar da na aukar a kanku.
11 Kada ku ji tsoron sarkin Babilon, wanda kuke tsoro a yanzu. Kada ku ji tsoronsa,
in ji Ubangiji, gama ina tare da ku zan kuma cece ku daga hannuwansa. 12 Zan nuna
muku jinƙai don yă nuna muku jinƙai ya kuma maido da ku ƙasarku.'

13 "Amma fa, in kuka ce, 'Ba za mu zauna a wannan ƙasa ba,' ta haka kuka kuma
nuna rashin biyayya ga Ubangiji Allahnku, 14 in kuma kuka ce, 'A'a, za mu tafi mu
zauna a Masar, inda ba za mu ga yaƙi ko mu ji ƙarar ƙaho ko mu ji yunwa ba,' 15 to,
ku ji maganar Ubangiji, ya raguwar Yahuda. Ga abin da Ubangiji Maɗaukaki, Allah
na Isra'ila, yana cewa, 'In kun ƙudura ku tafi Masar kuka kuma tafi kun zauna a
can, 16 takobin da kuke tsoro zai same ku a can, kuma yunwar da kuke tsoro za tă bi
ku zuwa Masar, a can kuwa za ku mutu. 17 Tabbatacce, duk waɗanda suka ƙudura
suka tafi Masar su zauna a can za su mutu ta wurin takobi, yunwa da annoba; ba
ko ɗayansu zai tsira ko ya kuɓuta wa masifar da zan aukar a kansu.' 18 Ga abin da
Ubangiji Maɗaukaki, Allah na Isra'ila, yana cewa, 'Kamar yadda na kwararo fushina
da hasalata a kan mazaunan Urushalima, haka kuma zan kwararo fushina a kanku
sa'ad da kuka tafi Masar. Za ku zama abin la'ana da abin tsoro, abin ƙyama da abin
ba'a; ba za ku ƙara ganin wannan wuri ba.'

19 "Ya ku raguwar Yahuda, Ubangiji ya ce muku, 'Kada ku je Masar.' Ku tabbatar
da wannan. Na gargaɗe ku yau 20 cewa in kun yi kuskure† sa'ad da kuka aike ni
wurin Ubangiji Allahnku kuka kuma ce, 'Yi mana addu'a ga Ubangiji Allahnmu; ka
faɗa mana duk abin da ya faɗa za mu kuwa aikata.' 21 Na faɗa muku yau, amma
har yanzu ba ku yi biyayya ga Ubangiji Allahnku cikin dukan abin da ya aiko ni in
faɗa muku ba. 22 Saboda haka yanzu, ku tabbatar da wannan. Za ku mutu ta wurin
takobi, yunwa da annoba a wurin da kuke so ku tafi ku zauna."

* **42:1** Ibraniyanci; Seftuwajin (dubi kuma Irm 43.2) Azariya † **42:20** Ko kuwa kun yi kuskure a zukatanku

# 43

1 Sa'ad da Irmiya ya gama faɗa wa mutane dukan maganar UBANGIJI Allahnsu, duk
abin da UBANGIJI ya aike shi ya faɗa musu, 2 Azariya ɗan Hoshahiya da Yohanan
ɗan Kareya da dukan masu ɗaga kai suka ce wa Irmiya, "Kana ƙarya ne! UBANGIJI
Allahnmu bai aike ka ka ce, 'Kada ku tafi Masar don ku zauna a can.' 3 Amma Baruk
ɗan Neriya yana zuga ka a kanmu don ka ba da mu ga Babiloniyawa, don su kashe
mu ko su kai mu zaman bauta a Babilon."
4 Saboda haka Yohanan ɗan Kareya da dukan shugabannin sojoji da dukan mutane
suka yi rashin biyayya ga umarnin UBANGIJI da su zauna a ƙasar Yahuda. 5 A
maimako, Yohanan ɗan Kareya da dukan shugabannin sojoji suka kwashe raguwar
Yahuda waɗanda suka dawo su zauna a ƙasar Yahuda daga dukan al'umman inda
aka kora su. 6 Suka kuma kwashe dukan maza, mata da yara da 'ya'yan sarki
mata waɗanda Nebuzaradan shugaban matsaran sarki ya bari tare da Gedaliya ɗan
Ahikam, ɗan Shafan, da Irmiya annabi da kuma Baruk ɗan Neriya. 7 Saboda haka
suka shiga Masar cikin rashin biyayya ga UBANGIJI suka tafi har can Tafanes.
8 A Tafanes maganar UBANGIJI ta zo wa Irmiya cewa, 9 "Yayinda Yahudawa suna
kallo, ka ɗauki waɗansu manyan duwatsu tare da kai ka kuma binne su cikin yumɓu
a tubalin dakalin ƙofar shiga fadar Fir'auna a Tafanes. 10 Sa'an nan ka faɗa musu
cewa, 'Ga abin da UBANGIJI Maɗaukaki, Allah na Isra'ila, yana cewa, zan aika wa
bawana Nebukadnezzar sarkin Babilon, zan kuma sa kursiyinsa a kan waɗannan
duwatsun da na binne a nan; zai fadada bukkar mulkinsa a bisansu. 11 Zai zo ya yaƙi
Masar, ya kawo mutuwa ga waɗanda aka ƙaddara musu mutuwa, zaman bauta ga
waɗanda aka ƙaddara musu zaman bauta, da kuma takobi ga waɗanda aka ƙaddara
su mutu ta takobi. 12 Zai* sa wuta wa haikalan allolin Masar; zai ƙone haikalansu yă
kuma kwashe allolinsu bayi. Kamar yadda makiyayi yakan yafa mayafinsa kewaye
da shi, haka zai yafa Masar kewaye da kansa ya kuma tashi a wurin babu abin da
ya same shi. 13 A can cikin haikalin rana† a Masar zai rushe al'amudan duwatsu yă
kuma ƙone haikalan allolin Masar.' "

# 44

*Masifa domin bautar gumaka*

1 Wannan maganata zo wa Irmiya game da dukan Yahudawa masu zama a Masar ta
Kasa, a Migdol, Tafanes da Memfis, da kuma a Masar ta Bisa. 2 "Ga abin da UBANGIJI
Maɗaukaki, Allah na Isra'ila yana cewa kun ga masifa mai girmar da na kawo a kan
Urushalima da kuma a kan dukan garuruwan Yahuda. A yau sun zama hamada da
kuma kango 3 saboda muguntar da suka aikata. Sun tsokane ni na yi fushi ta wurin
ƙone turare da kuma ta wurin bauta wa waɗansu allolin da su ko ku ko kakanninku
ba su taɓa sani ba. 4 Sau da sau na aiki bayina annabawa, waɗanda suka ce, 'Kada ku
yi wannan abin ƙyama da na ƙi!' 5 Amma ba su saurara ko su kasa kunne ba; ba su
juye daga muguntarsu ko su daina ƙone turare wa waɗansu alloli ba. 6 Saboda haka,
fushina mai ƙuna ya fāɗo a kan garuruwan Yahuda da kuma titunan Urushalima na
kuma mai da su kufai da suke a yau.
7 "To, ga abin da UBANGIJI Allah Maɗaukaki, Allah na Isra'ila, yana cewa don me
kuka kawo irin masifa mai girma haka a kanku ta wurin warewa daga Yahuda maza
da mata, yara da jarirai, kun kuma bar kanku babu raguwa? 8 Me ya sa kuka tsokane
ni in yi fushi saboda abin da hannuwanku suka yi, kuna ƙone turare wa waɗansu
alloli a Masar, inda kuka zo don ku zauna? Za ku hallakar da kanku ku kuma mai da
kanku abin la'ana da abin zargi da abin ba'a a cikin dukan al'umman duniya. 9 Kun
manta mugayen ayyukan kakanninku, da na sarakuna da sarauniyoyin Yahuda da

* **43:12** Ko kuwa Zan † **43:13** Ko kuwa a Heliyofolis

mugayen ayyukanku, da na matanku a cikin Yahuda da kan titunan Urushalima?
10 Har yǎ zuwa yau ba su ƙasƙantar da kansu ko su nuna bangirma, ko su kiyaye
dokata da ƙa'idodin da na sa a gabanku da kakanninku ba.

11 "Saboda haka ga abin da UBANGIJI Maɗaukaki, Allah na Isra'ila, yana cewa na
ƙudura in aukar muku da masifa in kuma hallaka dukan Yahuda. 12 Zan ɗauke
raguwar Yahuda waɗanda suka ƙudurta su je Masar su zauna a can. Duk za su
hallaka a Masar; za su mutu ta wurin takobi ko su mutu da yunwa. Daga ƙarami
zuwa babba, za su mutu ta wurin takobi ko yunwa. Za su zama abin zarge da abin
tsoro, abin la'ana da abin ba'a. 13 Zan hukunta waɗanda suke zama a Masar da
takobi, yunwa da annoba, yadda na hukunta Urushalima. 14 Babu wani daga raguwar
Yahuda wanda ya tafi Masar da zai kuɓuta ko ya tsira har ya komo zuwa ƙasar
Yahuda, wadda za su yi marmari su komo su zauna; babu wani da zai komo sai dai
'yan gudun hijira."

15 Sai dukan mazan da suka san cewa matansu suna ƙone turare wa waɗansu alloli,
tare da dukan matan da suke a nan babban taro, da kuma dukan mutanen da suke
zama a Masar ta Kasa da ta Bisa, suka ce wa Irmiya, 16 "Ba za mu saurari saƙon da
ka yi mana magana a sunan UBANGIJI ba! 17 Lalle za mu aikata duk abin da muka ce
za mu yi. Za mu ƙone turare ga Sarauniyar Sama za mu kuma miƙa hadayun sha
gare ta kamar dai yadda mu da kakanninmu, sarakunanmu da fadawanmu muka yi
a garuruwan Yahuda da kuma kan titunan Urushalima. A lokacin muna da abinci a
yalwace muna kuma da arziki ba mu kuma da wata damuwa. 18 Amma tun da muka
daina ƙone turare ga Sarauniyar Sama da kuma miƙa mata hadayun sha, muka rasa
kome muna ta mutuwa ta wurin takobi da yunwa."

19 Matan suka ƙara da cewa, "Sa'ad da muka ƙone turare ga Sarauniyar Sama muka
kuma miƙa mata hadayun sha, mazanmu ba su san muna yin waina kamar siffarta
muna kuma miƙa mata hadayun sha ba?"

20 Sai Irmiya ya ce wa dukan mutanen, maza da mata, waɗanda suke ba shi amsa,
21 "UBANGIJI bai tuna ya kuma yi tunani game da turaren da aka ƙone a garuruwan
Yahuda da kan titunan Urushalima wanda ku da kakanninku, sarakunanku da
fadawanku da mutanen ƙasar ba ne? 22 Sa'ad da UBANGIJI bai iya jurewa da mugayen
ayyukanku da kuma abubuwa banƙyama da kuka aikata ba, sai ƙasarku ta zama
abin la'ana da kufai babu mazauna yadda yake a yau. 23 Domin kun ƙone turare
kuka kuma yi wa UBANGIJI zunubi ba ku kuma yi masa biyayya ko ku kiyaye dokarsa
ko ƙa'idodinsa ko farillansa ba, wannan masifa ta aukar muku, yadda yanzu kuka
gani."

24 Sai Irmiya ya ce wa dukan mutane, har da mata, "Ku saurari maganar UBANGIJI,
dukanku mutanen Yahuda a Masar. 25 Ga abin da UBANGIJI Maɗaukaki, Allah na
Isra'ila, yana cewa ku da matanku kun nuna ta wurin ayyukanku abin da kuka yi
alkawari sa'ad da kuka ce, 'Lalle za mu yi abin da muka yi alkawari na ƙone turare
da kuma miƙa hadayun sha ga Sarauniyar Sama.'

"To, sai ku ci gaba, ku aikata abin da kuka yi alkawari! Ku cika alkawarinku!
26 Amma ku ji maganar UBANGIJI, dukan Yahudawan da suke zama a Masar, 'Na rantse
da sunana,' in ji UBANGIJI, 'cewa babu wani daga Yahuda wanda yake zama a ko'ina
a Masar zai ƙara kira bisa sunana ko ya rantse ya ce, "Muddin UBANGIJI Mai Iko Duka
yana raye." 27 Gama ina lura da su don lahani, ba alheri ba; mutanen Yahuda da suke
a Masar za su hallaka ta wurin takobi da yunwa sai dukansu sun hallaka. 28 Waɗanda
suka kuɓuta wa takobi suka komo zuwa ƙasar Yahuda daga Masar za su zama kima
kawai. Sa'an nan dukan raguwar Yahuda waɗanda suka zo don su yi zama a Masar
za su san maganar wane ne za tǎ tabbata, tawa ko tasu.

29 " 'Wannan zai zama alama a gare ku cewa zan hukunta ku a wannan wuri,'
in ji UBANGIJI, 'saboda ku san cewa barazanata ta lahani a kanku tabbatacce za tă
cika.' 30 Ga abin da UBANGIJI yana cewa, 'Zan bayar da Fir'auna Hofra sarkin Masar
ga abokan gābansa waɗanda suke neman ransa, kamar yadda na ba da Zedekiya
sarkin Yahuda ga Nebukadnezzar sarkin Babilon, abokin gāban da ya nemi ransa.' "

# 45

## *Saƙo zuwa ga Baruk*

1 Ga abin da Irmiya annabi ya faɗa wa Baruk ɗan Neriya a shekara ta huɗu ta
Yehohiyakim ɗan Yosiya sarkin Yahuda, bayan Baruk ya rubuta maganar da Irmiya
ya shibta masa a kan littafi cewa, 2 "Ga abin da UBANGIJI, Allah na Isra'ila, yana ce
maka, Baruk. 3 Ka ce, 'Kaitona! UBANGIJI ya ƙara baƙin ciki da wahalata; na gaji da
nishe-nishe ban kuma huta ba.' " 4 UBANGIJI ya ce, "Ka faɗa masa wannan, 'Ga abin
da UBANGIJI yana cewa, zan rushe abin da na gina in kuma tumɓuke abin da na dasa,
a duk fāɗin ƙasar. 5 Ya kamata ka nemi manyan abubuwa wa kanka? Kada ka neme
su. Gama zan aukar da masifa a kan dukan mutane, in ji UBANGIJI, amma duk inda
ka tafi zan bar ka ka kuɓutar da ranka.' "

# 46

## *Saƙo game da Masar*

1 Ga maganar UBANGIJI da ta zo wa Irmiya annabi game da al'ummai.

2 Game da Masar.

Ga saƙo game da sojojin Fir'auna Neko sarkin Masar, wanda Nebukadnezzar sarkin Babilon ya ci da yaƙi a Karkemish a Kogin Yuferites a shekara ta huɗu ta Yehohiyakim ɗan Yosiya sarkin Yahuda.

3 "Ku shirya garkuwoyinku, manya da ƙanana,
ku kuma fito don yaƙi!
4 Ku shirya dawakai,
ku sa musu sirdi!
Ku tsaya a wurarenku
saye da hulunan kwano a kai!
Ku wasa māsunku,
ku yafa kayan yaƙinku!
5 Me nake gani?
Sun tsorata,
suna ja da baya,
an ci jarumawansu.
Suna gudu da sauri
ba waiwayawa,
akwai razana a kowane gefe,"
in ji UBANGIJI.
6 "Masu saurin gudu ba sa iya gudu
haka ma masu ƙarfi ba sa iya kuɓuta.
A arewa ta Kogin Yuferites
sun yi tuntuɓe sun fāɗi.

7 "Wane ne wannan mai tashi kamar Nilu,
kamar koguna masu tafasar ruwaye?

8 Masar tana tashi kamar Nilu,
kamar koguna masu tafasa.
Tana cewa, ‘Zan tashi in rufe duniya;
zan hallakar da birane da kuma mutanensu.’
9 Ku yi sukuwar hauka, ya dawakai!
Ku tashi a guje, ya mahayan kekunan yaƙi!
Ku yi ta fitowa, ya jarumawa,
mutanen Kush da kuma Ludim masu riƙon garkuwoyi,
mutanen Lidiya, masu iya jan baka.
10 Amma wannan rana ta Ubangiji, UBANGIJI Maɗaukaki
ranar ɗaukar fansa, gama ɗaukar fansa a kan maƙiyansa.
Takobi zai yi ta ci sai ya gamsu,
sai ya kashe ƙishirwansa da jini.
Gama Ubangiji, UBANGIJI Maɗaukaki, zai miƙa hadaya
a ƙasar arewa kusa da Kogin Yuferites.

11 “Ki haura Gileyad ki samo magani,
Ya Budurwa ’Yar Masar.
Amma kin riɓanya magani a banza;
ba magani dominki.
12 Al’ummai za su ji game da kunyar da kika sha;
kukanki zai cika duniya.
Jarumi zai yi tuntuɓe a kan wani;
dukansu biyu za su fāɗi tare.”
13 Ga saƙon da UBANGIJI ya yi wa Irmiya annabi game da zuwan Nebukadnezzar
sarkin Babilon don yă yaƙi Masar.
14 “Ka yi shelar wannan a Masar, ka kuma furta shi a Migdol;
ka yi shelarsa kuma a Memfis da Tafanes.
‘Ku ɗauki matsayinku ku kuma shirya,
gama takobi na cin waɗanda suke kewaye da ku.’
15 Me zai sa a wulaƙanta jarumawanka haka?
Ba za su iya tsayawa ba, gama UBANGIJI zai ture su ƙasa.
16 Za su yi ta tuntuɓe;
za su fāɗi akan juna.
Za su ce, ‘Mu tashi, mu koma
zuwa wurin mutanenmu da kuma ƙasashenmu,
daga takobin masu danniya.’
17 A can za su tā da murya su ce,
‘Fir’auna sarkin Masar mai yawan surutu ne kawai;
ya bar zarafi ya wuce masa.’

18 “Muddin ina raye,” in ji Sarki,
wanda sunansa ne UBANGIJI Maɗaukaki,
“wani zai ɓullo wanda yake kamar Tabor a cikin duwatsu,
kamar Karmel kusa da teku.
19 Ku tattara kayanku don shirin zuwa zaman bauta,
ku da kuke zama a Masar,
gama Memfis za tă zama kufai
ta zama kango, babu mazauna.

20 “Masar kyakkyawar karsana ce,

amma bobuwa tana zuwa a kanta daga arewa.
21 Sojojin da ta yi hayarsu a cikinta
suna kamar ’yan maruƙa masu kitse.
Su ma za su juya su kuma gudu gaba ɗaya,
ba za su iya tsayawa ba,
gama ranar masifa tana zuwa a kansu,
lokacin da za su sha hukunci.
22 Masar za tă yi huci kamar macijin da yake gudu
yayinda abokin gāba yana matsowa da ƙarfi;
za su fāɗo mata gatura
kamar mutanen da suke saran itatuwa.
23 Za su sari kurminta,” in ji UBANGIJI,
“ko da yake yana maƙare da itatuwa.
Sun fi fāra yawa,
ba su ƙidayuwa.
24 Za a kunyatar da Diyar Masar,
da aka bashe ga mutanen arewa.”
25 UBANGIJI Maɗaukaki, Allah na Isra’ila, yana cewa, “Ina gab da kawo hukunci a
kan allahn Amon na Tebes,* a kan Fir’auna, a kan Masar da allolinta da sarakunanta,
da kuma a kan waɗanda suka dogara ga Fir’auna. 26 Zan ba da su ga waɗanda suke
neman ransu, ga Nebukadnezzar sarkin Babilon da fadawansa. Amma daga baya,
Masar za tă kasance da mazauna kamar dā,” in ji UBANGIJI.
27 “Kada ka ji tsoro, ya Yaƙub bawana;
kada ka karai, ya Isra’ila.
Tabbatacce zan cece ka daga wuri mai nisa,
zuriyarka daga ƙasar bautarsu.
Yaƙub zai sāke kasance cikin salama, rai kwance,
babu kuma wanda zai sa ya ji tsoro.
28 Kada ka ji tsoro, ya Yaƙub bawana,
gama ina tare da kai,” in ji UBANGIJI.
“Ko da na hallaka dukan al’ummai sarai
inda na kora ka, ba zan hallaka ka sarai ba.
Zan hore ka amma da adalci kaɗai;
ba zan bar ka ba hukunci ba.”

# 47

### *Saƙo game da Filistiyawa*

1 Ga maganar UBANGIJI da ta zo wa Irmiya annabi game da Filistiyawa kafin
Fir’auna ya yaƙi Gaza.

2 Ga abin da UBANGIJI yana cewa,
“Dubi yadda ruwaye suna tasowa a arewa;
za su zama kogi mai rigyawa.
Za su malala a ƙasa da kuma a kan kome da yake cikinta,
garuruwa da waɗanda suke zaune a cikinsu.
Mutane za su yi kuka;
dukan mazaunan ƙasar za su yi kururuwa
3 da jin motsin takawar kofatan dawakai,
da jin surutun kekunan yaƙin abokin gāba
da motsin ƙafafunsu.

* **46:25** Da Ibraniyanci No

Ubanni ba za su juye don su taimaki ’ya’yansu ba;
hannuwansu za su yi laƙwas.
4 Gama rana ta zo
da za a hallaka Filistiyawa
a kuma datse dukan waɗanda suka ragu
waɗanda za su iya taimakon Taya da Sidon.
UBANGIJI yana gab da hallaka Filistiyawa,
raguwa daga bakin tekun Kaftor.
5 Gaza za tă aske kanta cikin baƙin ciki;
Ashkelon zai yi shiru.
Ya raguwar da suke zama a fili,
har yaushe za ku tsattsage kanku?

6 “Za ku yi kuka kuna cewa, ‘Wayyo, takobin UBANGIJI
sai yaushe za ka huta?
Ka koma kubenka;
ka huta, ka yi shiru.’
7 Amma ta yaya zai huta
sa’ad da UBANGIJI ya umarta,
sa’ad da ya umarta shi
don yă faɗa wa Ashkelon da kuma bakin teku?”

# 48

*Saƙo game da Mowab*

1 Game da Mowab.

Ga abin da UBANGIJI Maɗaukaki, Allah na Isra’ila, yana cewa,
“Kaito ga Nebo, gama za tă lalace.
Kiriyatayim za su kunyata a kuma kame ta;
katagar* za tă sha kunya ta kuma wargaje.
2 Ba za a ƙara yabi Mowab ba;
a Heshbon† mutane za su shirya mata maƙarƙashiya.
‘Zo, mu tafi mu kawo ƙarshe ga wannan al’umma.’
Ke kuma, ya Madmen‡ za ki yi shiru;
takobi zai fafare ki.
3 Saurari kuka daga Horonayim,
kukan risɓewa mai girma da hallaka.
4 Za a karye Mowab;
ƙanananta za su yi kuka.
5 Sun haura hanyar zuwa Luhit,
suna kuka mai zafi yayinda suke tafiya;
a hanyar da ta gangara zuwa Horonayim
suna kuka a kan hallakar da aka ji.
6 Ku gudu! Ku gudu don tserar da ranku;
ku zama kamar kurmi§ a hamada.
7 Da yake kun dogara ga ayyukanku da arzikinku,
ku ma za a kwashe ku bayi,
Kemosh zai tafi bauta,

* **48:1** Ko kuwa / Misgab † **48:2** Da Ibraniyanci na Heshbon ya yi kamar Ibraniyanci na maƙarƙashiya. ‡ **48:2** Sunan garin Mowab nan Madmen ya yi kamar Ibraniyanci na yi shiru. § **48:6** Ko kuwa kamar Arower

tare da firistocinsa da fadawansa.
8 Mai hallakarwa zai aukar wa kowane gari,
kuma ba wani garin da zai kuɓuta.
Kwari zai lalace
tudu kuma ya hallaka,
domin UBANGIJI ya faɗa.
9 Ku sa gishiri a kan Mowab,
gama za tă zama kango;*
garuruwanta za su zama kufai,
ba mazauna a cikinsu.

10 "La'ananne ne shi wanda yake sake a yin aikin UBANGIJI!
La'ananne ne wanda ya janye takobinsa daga zub da jini!

11 "Mowab ta kasance cikin kwanciyar rai tun ƙuruciyarta,
kamar ruwan inabin da aka bari lis,
ba a juya daga tulu zuwa wani tulu ba
ba tă tafi bauta ba.
Saboda haka tana da ɗanɗanonta,
kuma ƙanshinta bai canja ba.
12 Kwanaki suna zuwa," in ji UBANGIJI,
"sa'ad da zan aika da mutanen da za su tuntsurar da tuluna,
su kuma zubar da ita waje.
Za su bar tulunan ba kome a ciki
su kuma farfashe tulunanta.
13 Sa'an nan Mowab za tă ji kunyar Kemosh,
yadda gidan Isra'ila ya ji kunya
sa'ad da suka dogara ga Betel.

14 "Yaya za ku ce, 'Mu jarumawa ne,
mutane masu ƙarfi a yaƙi?'
15 Mowab za tă hallaka a kuma kai wa garuruwanta hari;
samarinta kyawawa za su gangara cikin mayanka,"
in ji Sarki, wanda sunansa UBANGIJI Maɗaukaki ne.
16 "Fāɗuwar Mowab ta yi kusa;
bala'inta zai auku nan da nan.
17 Yi kuka saboda ita, dukanku mazaunan kewayenta,
duk waɗanda suka san shahararta;
ku ce, 'Dubi yadda sandan sarauta mai iko ya karye,
dubi yadda sanda mai daraja ya karye!'

18 "Sauko daga darajarku
ku zauna a busasshiyar ƙasa,
Ya mazaunan Diyar Dibon,
gama shi mai hallaka Mowab
zai haura a kanku
zai kuma lalace biranenku masu kagarai.
19 Ku tsaya a bakin hanya ku duba,
ku da kuke zama a Arower.
Ku tambayi mutumin da yake gudu da macen da take tserewa,
tambaye su, 'Me ya faru?'

* **48:9** Ko kuwa Ku ba wa Mowab fikafikai, don tă tashi tă tafi

20 An kunyata Mowab, gama ta wargaje.
Ku yi kuka ku kuma tā da murya!
Ku yi shela kusa da Arnon
cewa an hallaka Mowab.
21 Hukunci ya zo wa tudu,
zuwa Holon, Yahza da Mefa'at,
22 zuwa Dibon, Nebo da Bet-Dibilatayim,
23 zuwa Kiriyatayim, Bet-Gamul da Bet-Meyon,
24 zuwa Keriyot da Bozra
zuwa dukan garuruwan Mowab, nesa da kusa.
25 An karye ƙahon Mowab;
an karye hannunta,"
in ji UBANGIJI.

26 "Ku bugar da ita
domin ta tayar wa UBANGIJI.
Bari Mowab tă yi ta birgima a cikin amanta;
bari tă zama abin dariya.
27 Isra'ila ma bai zama abin dariya a gare ki ba?
Ba a kama shi cikin ɓarayi,
har kaɗa kai na ba'a kike yi
a duka sa'ad da kike magana game da shi?
28 Ku bar garuruwanku ku zauna a cikin duwatsu,
ku da kuke zama a Mowab.
Ku zama kamar kurciyar da take sheƙarta
a bakin kogo.

29 "Mun ji labarin girman kan Mowab
mun ji alfarma girmankanta da kumburinta
girmankanta da fariyarta
da renin zuciyarta.
30 Na san alfarmanta amma a banza ne," in ji UBANGIJI,
"kuma taƙamarta ba ya cimma kome.
31 Saboda haka zan yi kuka a kan Mowab
gama dukan Mowab zan yi kuka,
Zan yi gurnani don mutanen Kir Hareset.
32 Zan yi kuka saboda kai, yadda Yazer ya yi kuka
Ya kuringar Sibma.
Rassanki sun kai har teku;
sun kai har tekun Yazer.
Mai hallakarwa ya faɗo
a kan 'ya'yan itatuwanku da kuma inabinku da suka nuna.
33 Farin ciki da murna su ɓace
daga lambunan itatuwa da kuma gonakin Mowab.
Na dakatar da malalar ruwan inabi daga wurin matsi;
ba wanda zai matse su da ihun farin ciki.
Ko da yake akwai sowa
sowar ba ta farin ciki ba ce.

34 "Muryar kukansu na tashi
daga Heshbon zuwa Eleyale da Yahaz,

daga Zowar har zuwa Horonayim da Eglat Shelishiya,
gama har ruwan Nimrim ma sun bushe.
35 A Mowab zan kawo ƙarshen
waɗanda suke miƙa hadayu a masujadan kan tudu
suna kuma ƙone turare ga allolinsu,"
in ji UBANGIJI.
36 "Saboda haka zuciyata na makoki don Mowab kamar busa;
tana makoki kamar busa saboda mutanen Kir Hareset.
Arzikin da suka samu ta ƙare.
37 An aske kowane kai
aka kuma yanke kowane gemu
aka kuma sa wa kowane kwankwaso rigar makoki.
38 A kan dukan rufi a Mowab
da kuma a dandalin jama'a
babu wani abu sai kuka
gama na karye Mowab
kamar tulun da babu mai so,"
in ji UBANGIJI.
39 "Duba yadda aka ragargazar ta ita! Duba yadda suke kuka!
Duba yadda Mowab ta juya bayanta da kunya!
Mowab ta zama abin ba'a
abin tsoro ga dukan waɗanda suke kewaye da ita."
40 Ga abin da UBANGIJI yana cewa,
"Ga shi! Gaggafa tana firiya zuwa ƙasa,
tana shimfiɗa fikafikanta a kan Mowab.
41 Za a ci Keriyot†
a kuma kame kagarai.
A wannan rana zukatan jarumawan Mowab
za su zama kamar zuciyar macen da take naƙuda.
42 Za a hallakar da Mowab a matsayin al'umma
domin ta tayar wa UBANGIJI.
43 Razana da rami da tarko suna jiranku,
Ya mutanen Mowab,"
in ji UBANGIJI.
44 "Duk wanda ya gudu daga razana
zai fāɗa cikin rami,
duk wanda ya haura daga rami
zai fāɗa cikin tarko;
gama zan kawo wa Mowab
shekarar hukuncinta,"
in ji UBANGIJI.

45 "A ƙarƙashin Heshbon
masu gudun hijira suna tsaye ba mai taimako,
gama wuta ta mutu daga Heshbon,
harshen wuta daga tsakiyar Sihon;
ta ƙone goshin Mowab,
ƙoƙon kai na 'yan tayarwa masu surutu.
46 Kaitonki, ya Mowab!
Mutanen Kemosh sun hallaka;
an kai 'ya'yanki maza daurin talala

† **48:41** Ko kuwa Birane

'ya'yanki mata zaman bauta.

47 "Duk da haka zan maido da wadatar Mowab
a kwanaki masu zuwa,"
in ji UBANGIJI.
A nan hukuncin Mowab ya ƙare.

# 49

*Saƙo game da Ammon*

1 Game da Ammonawa.

Ga abin da UBANGIJI yana cewa,
"Isra'ila ba shi da 'ya'ya maza ne?
Ba shi da magāda ne?
To, me ya sa Molek* ya mallaki Gad?
Me ya sa mutanensa suka zama a garuruwansa?
2 Amma kwanaki suna zuwa,"
in ji UBANGIJI,
"sa'ad da zan yi kirarin yaƙi
a kan Rabba ta Ammonawa;
zai zama tarin juji,
za a sa wuta a ƙauyukan da suke kewayenta.
Sa'an nan Isra'ila zai kori
waɗanda suka kore shi,"
in ji UBANGIJI.
3 "Ki yi kuka, ya Heshbon, gama an hallaka Ai!
Ku tā da murya ku yi kuka, ya mazaunan Rabba!
Ku sa tufafin makoki;
ku ruga nan da can a cikin katanga,
gama Molek zai tafi bauta,
tare da firistocinsa da kuma fadawansa.
4 Me ya sa kuke taƙama da kwarurukanku,
taƙama da kwarurukanku masu amfani?
Ya ke diya marar aminci,
kin dogara a wadatarki kika kuma ce,
'Wa zai iya fāɗa mini?'
5 Zan kawo razana a kanki
daga waɗanda suke kewaye da ke,"
in ji UBANGIJI Maɗaukaki.
"Za a kore kowannenku,
babu wani da zai tattara masu gudun hijira.

6 "Duk da haka, daga baya, zan maido da wadatar Ammonawa,"
in ji UBANGIJI.

*Saƙo game da Edom*

7 Game da Edom.

Ga abin da UBANGIJI Maɗaukaki yana cewa,
"Babu sauran hikima a Teman ne?

* **49:1** Ko kuwa sarkinsu; Da Ibraniyanci malkam; haka ma a aya 3.

Shawara ta ɓace daga masu basira ne?
Hikimarsu ta ruɓe ne?
8 Ku juya ku gudu, ku ɓuya a cikin kogwanni masu zurfi,
ku da kuke zama a Dedan,
gama zan kawo masifa a kan Isuwa
a lokacin da zan hukunta shi.
9 In masu tsinkar ʼyaʼyan inabi suka zo maka,
ba za su rage ʼyaʼyan inabi kaɗan ba?
In ɓarayi suka zo da dare,
ba za su sata abin da kawai suke bukata ba?
10 Amma zan washe Isuwa sarai;
zan bubbuɗe wuraren ɓuyarsa,
don kada yă ɓoye kansa.
ʼYaʼyansa, danginsa da maƙwabtansa za su hallaka,
ba kuwa zai ƙara kasancewa ba.
11 Ka bar marayunka; zan tsare ransu.
Gwaurayenka kuma za su dogara a gare ni.”

12 Ga abin da Ubangiji yana cewa, “In waɗanda ba su dace su sha kwaf ɗin ba suka
sha shi, me ya sa za ka kuɓuta? Ba za ka kuɓuta ba, sai ka sha shi. 13 Na rantse da
kaina,” in ji Ubangiji, “cewa Bozra za tă zama kufai da kuma abin tsoro, abin dariya
da abin laʼana; kuma dukan garuruwanta za su kasance kufai har abada.”
14 Na ji saƙo daga Ubangiji cewa;
an aiki jakada zuwa ga alʼummai ya ce,
“Ku tattara kanku don ku fāɗa mata!
Ku tashi don yaƙi!”

15 “Yanzu zan mai da kai ƙanƙani a cikin alʼummai
abin reni a cikin mutane.
16 Tsoron da ka sa ake ji
da kuma girman kan zuciyarka ya ruɗe ka,
kai da kake zama a kogon dutse,
kai da kake kan tudu.
Ko da yake ka gina wa kanka sheƙa can bisa kamar na gaggafa,
daga can zan sauko da kai ƙasa,”
in ji Ubangiji.
17 “Edom za tă zama abin tsoro;
dukan wanda ya wuce zai giggice ya yi tsaki
saboda dukan mikinta.
18 Kamar yadda aka tumɓuke Sodom da Gomorra,
tare da garuruwan da suke maƙwabtaka da su,”
in ji Ubangiji,
“haka ba wanda zai zauna a can;
ba wani da zai zauna a cikinta.

19 “Kamar zaki mai haurawa daga kurmin Urdun
zuwa wurin kiwo mai kyau,
zan kori Edom daga ƙasarta nan da nan.
Wane ne zaɓaɓɓen da zan naɗa don wannan?
Wane ne yake kama da ni kuma wa zai kalubalance ni?
Kuma wane makiyayi ne zai yi gāba da ni?”

20 Saboda haka, ku ji abin da Ubangiji ya shirya a kan Edom,
abin da ya nufa wa waɗanda suke zama a Teman.

Za a ja ƙanana na garken tumaki a tafi;
zai hallaka wurin kiwonsu sarai saboda su.
21 Amon fāɗuwarsu zai sa ƙasa ta girgiza;
za a kuma ji muryar kukansu a Jan Teku.
22 Duba! Gaggafa tana firiya tana kuma saukowa,
tana buɗe fikafikanta a bisa Bozra.
A wannan rana zukatan jarumawan Edom
za su zama kamar macen da take naƙuda.

### *Saƙo game da Damaskus*

23 Game da Damaskus.
"Hamat da Arfad sun giggice,
gama sun ji mummunar labari.
Suna damuwa,
sun damu kamar tekun da baya hutu.
24 Damaskus ta karai
ta juya don ta gudu
tsoro kuma ya kama ta;
wahala da zafi sun kama ta,
zafi kamar na mace mai naƙuda.
25 Me ya sa ba a tafi aka bar sanannen birnin nan ba,
birnin da nake jin daɗi?
26 Tabbatacce, samarinta za su fāɗi a tituna;
dukan sojojinta za su yi shiru a wannan rana,"
in ji UBANGIJI Maɗaukaki.
27 "Zan cinna wa katangar Damaskus wuta;
za tă ci kagaran Ben-Hadad."

### *Saƙo game da Kedar da Hazor*

28 Game da Kedar da mulkokin Hazor, waɗanda Nebukadnezzar sarkin Babilon ya fāɗa wa.

Ga abin da UBANGIJI yana cewa,
"Tashi, ku fāɗa wa Kedar
ku kuma hallaka mutanen Gabas.
29 Za a ƙwace tentunansu da garkunansu;
za a tafi da mafakanta
tare da dukan kayayyakinsu da raƙumansu.
Mutane za su yi musu ihu,
'Razana ko'ina!'

30 "Ku yi maza ku gudu!
Ku zauna a kogo masu zurfi, ku da kuke zama a Hazor,"
in ji UBANGIJI.
"Nebukadnezzar sarkin Babilon ya shirya muku maƙarƙashiya;
ya ƙulla maƙarƙashiya a kanku.

31 "Ku tashi ku kuma fāɗa wa al'umma da sauƙi
wadda take zama da ƙarfin hali,"
in ji UBANGIJI,
"al'ummar da ba ta da ƙofofi ko ƙyamare;
mutanenta suna zama su kaɗai.
32 Za a washe raƙumansu,
garkunansu mai girma za su zama ganima.

Zan watsar da waɗanda suke a wurare masu nesa a ko'ina
zan kuma kawo musu masifa a kowane gefe,"
in ji UBANGIJI.
33 "Hazor za tă zama mazaunin diloli,
kufai har abada.
Ba wanda zai zauna a can;
ba wanda zai zauna a cikinta."

*Saƙo game da Elam*

34 Ga maganar UBANGIJI da ta zo wa Irmiya annabi game da Elam, a farkon mulkin
Zedekiya sarkin Yahuda.

35 Ga abin da UBANGIJI Maɗaukaki yana cewa,
"Ga shi, zan karye ƙarfin Elam,
zaunannen ƙarfinsu.
36 Zan kawo a kan Elam a kusurwoyi huɗu
daga kusurwoyi huɗu na duniya;
zan watsar da su zuwa kusurwoyi huɗu,
kuma ba al'ummar
da masu gudun hijirar Elam ba za su kai ba.
37 Zan ragargaza Elam a gaban maƙiyansu,
a gaban waɗanda suke neman ransu;
zan kawo masifa a kansu,
da zafin fushina,"
in ji UBANGIJI.
"Zan runtume su da takobi
sai na kawo ƙarshensu.
38 Zan sa kursiyina a Elam
in kuma hallaka sarkinta da fadawanta,"
in ji UBANGIJI.

39 "Duk da haka zan maido da wadatar Elam
a kwanaki masu zuwa,"
in ji UBANGIJI.

# 50

*Saƙo game da Babilon*

1 Ga maganar UBANGIJI da ya yi ta wurin Irmiya annabi game da Babilon da kuma
ƙasar Babiloniyawa.
2 "Ka yi shela ka kuma furta a cikin al'ummai,
ka tā da tuta ka kuma furta;
kada ku ɓoye kome, amma ku ce,
'Za a ci Babilon da yaƙi;
za a kunyata Bel,
Marduk ya cika da tsoro.
Siffofinta za su sha kunya
gumakanta za su cika da tsoro.'
3 Al'umma daga arewa za tă fāɗa mata
su mai da ƙasar kango.
Ba wanda zai zauna a cikinta;
mutane da dabbobi za su gudu.

4 “A kwanakin nan, a wannan lokaci,”
in ji UBANGIJI,
“mutanen Isra’ila da mutanen Yahuda gaba ɗaya
za su tafi cikin hawaye su nemi UBANGIJI Allahnsu.
5 Za su tambayi hanyar zuwa Sihiyona
su kuma juya fuskokinsu wajenta.
Za su zo su haɗa kansu ga UBANGIJI
a madawwamin alkawari
da ba za a manta da shi ba.

6 “Mutanena sun zama ɓatattun tumaki;
makiyayansu sun bauɗar da su
suka sa suna ta yawo a cikin duwatsu.
Sun yi ta yawo a bisa dutse da tudu
suka manta wurin hutunsu.
7 Duk wanda ya same su ya cinye su;
abokan gābansu suka ce, ‘Ba mu da laifi,
gama sun yi zunubi wa UBANGIJI, wurin kiwonsu na gaske,
UBANGIJI, abin sa zuciyar kakanninsu.’

8 “Ku gudu daga Babilon;
ku bar ƙasar Babiloniyawa,
ku zama kamar awakin da suke bi da garke.
9 Gama zan kuta in kuma kawo a kan Babilon
haɗinkan manyan al’ummai na arewa.
Za su ja dāgār gāba da ita,
kuma daga arewa za a ci ta da yaƙi.
Kibiyoyinsu za su zama kamar na gwanayen jarumawa
waɗanda ba sa dawowa hannu wofi.
10 Saboda haka za a washe Babiloniyawa;
dukan waɗanda suka washe ta za su ƙoshi,”
in ji UBANGIJI.

11 “Saboda kuna farin ciki kuna kuma murna,
ku da kuka washe gādona,
domin kuna tsalle kamar karsana mai sussuka hatsi
kuna kuma haniniya kamar ingarmu.
12 Mahaifiyarku za tă sha babbar kunya;
ita da ta haife ku za tă sha kunya.
Za tă zama mafi ƙanƙanta na al’ummai,
jeji, busasshiyar ƙasa, hamada.
13 Saboda fushin UBANGIJI ba za tă zauna a cikinta ba
amma za tă zama kufai gaba ɗaya.
Duk waɗanda suka wuce Babilon za su ji tsoro su kuma yi tsaki
saboda dukan mikinta.

14 “Ku ja dāgā kewaye da Babilon,
dukanku waɗanda kuke jan baka.
Ku harbe ta! Kada ku rage kibiyoyi,
gama ta yi zunubi ga UBANGIJI.
15 Ku yi kuwwa a kanta a kowane gefe!
Ta miƙa wuya, hasumiyarta ta fāɗi,

katangarta sun rushe.
Da yake wannan sakayya ce ta UBANGIJI,
ku ɗauki fansa a kanta;
yi mata yadda ta yi wa waɗansu.
16 Ku datse wa Babilon mai shuka,
da mai girbi lauje a lokacin girbi.
Saboda takobin mai zalunci
bari kowa ya koma ga mutanensa,
bari kowa ya gudu zuwa ga ƙasarsa.

17 “Isra’ila garke ne da ya watse
da zakoki suka kora.
Na farkon da ya cinye shi
sarkin Assuriya ne;
na ƙarshen da ya ragargaza ƙasusuwansa
Nebukadnezzar sarkin Babilon ne.”
18 Saboda haka ga abin da UBANGIJI Maɗaukaki, Allah na Isra’ila, yana cewa,
“Zan hukunta sarkin Babilon da ƙasarsa
yadda na hukunta sarkin Assuriya.
19 Amma zan komo da Isra’ila zuwa wurin kiwonsa
zai kuwa yi kiwo a Karmel da Bashan;
zai ƙosar da marmarinsa
a tuddan Efraim da Gileyad.
20 A kwanakin nan, da kuma a lokacin nan,”
in ji UBANGIJI,
“za a yi bincike don laifin Isra’ila,
amma ba za a samu ba,
kuma don zunubin Yahuda,
amma ba za a sami wani abu ba,
gama zan gafarta wa raguwar da na rage.

21 “Ku fāɗa wa ƙasar Meratayim
da waɗanda suke zama a Fekod.
Ku fafara, ku kashe kuma hallaka su sarai,”
in ji UBANGIJI.
“Ku aikata dukan abin da na umarce ku.
22 Hargowar yaƙi tana a ƙasar,
hargowar babbar hallaka!
23 Dubi yadda aka karya aka kuma ragargaza
gudumar dukan duniya!
Dubi yadda Babilon ta zama kufai
a cikin al’ummai!
24 Na sa miki tarko, Babilon,
kika kuwa kamu kafin ki sani;
aka same ki aka kuma kama ki
domin kin tayar wa UBANGIJI.
25 UBANGIJI ya buɗe taskar makamansa
ya fitar da makaman fushinsa,
gama Maɗaukaki UBANGIJI Mai Iko Duka yana da aikin da zai yi
a ƙasar Babiloniyawa.
26 Ku zo ku yi gāba da ita daga nesa.
Ku buɗe rumbunanta;
ku jibga ta kamar tsibin hatsi.

Ku hallaka ta sarai
kada ku bar mata raguwa.
27 Ku kashe dukan ʼyan bijimanta
bari su gangara zuwa mayanka!
Kaitonsu! Gama ranansu ta zo,
lokaci ya yi da za a hukunta su.
28 Ku saurari masu gudun hijira da masu neman mafaka daga Babilon
suna furtawa a Sihiyona
yadda UBANGIJI Allahnmu ya ɗauki fansa,
fansa domin haikalinsa.

29 "Ku kira ʼyan baka a kan Babilon,
dukan waɗanda suke jan baka.
Ku yi sansani kewaye da ita duka;
kada ku bar wani ya tsira.
Ku sāka mata don ayyukanta;
ku yi mata yadda ta yi.
Gama ta tayar wa UBANGIJI,
Mai Tsarkin nan na Israʼila.
30 Saboda haka, samarinta za su fāɗi a tituna;
za a kawar da dukan sojojinta a wannan rana,"
in ji UBANGIJI.
31 "Ga shi, ina gāba da ke, ya ke mai girman kai,"
in ji Ubangiji, UBANGIJI Maɗaukaki,
"gama ranarki ta zo,
lokacin da za a hukunta ki.
32 Mai ɗaga kai za tă yi tuntuɓe ta kuma fāɗi
kuma ba wanda zai taimake ta tă tashi;
zan hura wuta a garuruwanta
da za tă cinye duk waɗanda suke kewaye da ita."
33 Ga abin da UBANGIJI Maɗaukaki yana cewa,
"An danne mutanen Israʼila, haka ma mutanen Yahuda.
Dukan waɗanda suka kama su suna riƙe su kankan,
suna kin barinsu su tafi.
34 Duk da haka Mai Fansarsu yana da ƙarfi;
UBANGIJI Maɗaukaki ne sunansa.
Zai kāre muradunsu gabagadi
don yă kawo hutu ga ƙasarsu,
amma rashin hutu ga waɗanda suke zaune a Babilon.

35 "Akwai takobi a kan Babiloniyawa!"
In ji UBANGIJI
"a kan waɗanda suke zama a Babilon
da kuma a kan fadawanta da masu hikimarta!
36 Akwai takobi a kan annabawan ƙaryanta!
Za su zama wawaye.
Akwai takobi a kan jarumawanta!
Za su cika da tsoro.
37 Akwai takobi a kan dawakanta da kekunan yaƙinta
da kuma dukan baƙin da suke cikin mayaƙanta!
Za su zama mata.
Akwai takobi a kan dukiyarta!

Za a washe su.
38 Fāri a kan ruwanta!
Za su bushe ƙaf.
Gama ƙasa ce ta gumaka,
gumakan da za su haukace da tsoro.

39 “Saboda haka halittun hamada da kuraye za su zauna a can,
a can kuma mujiya za tă zauna.
Ba za a ƙara zauna
ko a yi zama a cikinta ba daga tsara zuwa tsara.
40 Yadda Allah ya tumɓuke Sodom da Gomorra
tare da maƙwabtan garuruwansu,”
in ji Ubangiji
“haka ma ba wanda zai zauna a can;
ba wani da zai zauna a cikinta.

41 “Duba! Ga sojoji suna zuwa daga arewa;
babbar al’umma da sarakuna masu yawa
suna tahowa daga iyakokin duniya.
42 Suna riƙe da baka da māshi;
mugaye ne marasa tausayi.
Amonsu ya yi kamar rurin teku
yayinda suke hawan dawakansu;
suna zuwa kamar mutane a dāgār yaƙi
don su fāɗa miki, ya Diyar Babilon.
43 Sarkin Babilon ya ji rahotanni game da su,
hannunsa kuma ya yi laƙwas.
Wahala ta kama shi,
zafi kamar na mace mai naƙuda.
44 Kamar zaki mai haurawa daga kurmin Urdun
zuwa wurin kiwo mai dausayi,
zan fafare Babilon daga ƙasan nan da nan.
Wane ne zaɓaɓɓen da zan naɗa domin wannan?
Wane ne kamar ni da zai kalubalance ni?
Kuma wanda makiyayi zai iya tsaya gāba da ni?”

45 Saboda haka, ku ji abin da Ubangiji ya shirya a kan Babilon,
abin da ya nufa gāba da ƙasar Babiloniyawa.
Za a kwashe ƙananan garkensu a tafi;
zai hallaka wurin kiwonsu sarai saboda su.
46 Da jin an ci Babilon da yaƙi sai duniya ta girgiza;
za a ji kukanta cikin al’ummai.

# 51

1 Ubangiji ya ce,
“Ga shi, zan zuga ruhun mai hallakarwa
a kan Babilon da mutanen Leb Kamai.
2 Zan aika da baƙi zuwa Babilon
su casa ta su kuma yi kaca-kaca da ƙasarta;
za su yi hamayya da ita a kowane gefe
a ranar masifarta.
3 Kada ku bar maharbi yă ja bakansa,
kada kuma ku bari yă sa kayan yaƙinsa.

Kada ku rage samarinta,
ku hallaka sojojinta ƙaf.
4 Za su fāɗi matattu a ƙasar Babilon,
da munanan raunuka a titunanta.
5 Gama UBANGIJI Maɗaukaki, Allah na Isra'ila da Yahuda
bai yashe su ba,
ko da yake ƙasarsu* cike da take da laifi
a gaban Mai Tsarki na Isra'ila.

6 "Ku gudu daga cikin Babilon!
Bari kowa yă ceci ransa!
Kada a hallaka saboda zunubanta.
Gama lokaci ne don ramuwar UBANGIJI,
zai sāka mata bisa ga alhakinta.
7 Babilon ta zama ƙoƙon zinariya a hannun UBANGIJI,
ta sa dukan duniya ta yi maye.
Kasashe sun sha ruwan inabinta,
saboda haka yanzu sun haukace.
8 Farat ɗaya Babilon za tă fāɗi ta farfashe.
Ku yi kuka dominta!
Ku samo mata magani saboda azabarta;
wataƙila za a iya warkar da ita.

9 " 'Da mun warkar da Babilon,
amma ba za tă warke ba;
mu ƙyale ta kowane yă koma garinsu,
gama hukuncinta ya kai sammai,
ya yi tsawo kamar gizagizai.'

10 " 'UBANGIJI ya baratar da mu;
zo mu tafi mu yi shelarsa a Sihiyona
mu faɗa abin da UBANGIJI Allahnmu ya yi.'

11 "Ku wasa kibiyoyi,
ku ɗauko garkuwoyi!
UBANGIJI ya zuga sarakunan Medes,
domin niyyarsa ce yă hallaka Babilon.
UBANGIJI zai yi ramuwa,
zai yi ramuwa saboda haikalinsa.
12 Ku tā da tuta gāba da katangan Babilon!
Ku ƙara matsara,
ku kafa masu tsaro,
ku shirya kwanto!
Ga shi, UBANGIJI zai aikata abin da ya faɗa
umarninsa a kan mutanen Babilon.
13 Ke da kike zama kusa da ruwaye
da kike kuma wadatar dukiya,
ƙarshenki ya zo,
lokaci ya yi da za a kau da ke.
14 UBANGIJI Maɗaukaki ya rantse da zatinsa, ya ce

* **51:5** Ko kuwa / kuma ƙasar Babiloniyawa

Tabbatacce zan cika ka da mutane kamar fāra,
za su kuwa yi sowa don nasara a kanka.

*(Irmiya 10.12-16)*

15 “Ya halicci ƙasa ta wurin ikonsa;
ya kafa duniya ta wurin hikimarsa,
ya kuma shimfiɗa sammai ta wurin fahiminsa.
16 Sa’ad da ya yi tsawa ruwan da suke sammai sukan yi ruri;
yakan sa gizagizai su tashi daga ƙarshen duniya.
Yakan tura walƙiya tare da ruwan sama
yakan kuma saki iska daga cikin taskokinsa.

17 “Kowane mutum marar azanci ne kuma ba shi da sani;
kowane maƙerin zinariya yakan sha kunya daga wurin gumakansa.
Siffofinsa na ƙarya ne;
babu numfashi a cikinsu.
18 Su marasa amfani ne, abubuwan ba’a ne kawai;
sa’ad da lokacin hukuncinsu ya kai, za su hallaka.
19 Wanda yake na wajen Yaƙub ba kamar waɗannan ba ne,
gama shi ne Mahalicci dukan abu,
har da kabilar abin gādonsa,
Ubangiji Maɗaukaki ne sunansa.

20 “Kai ne kulkin yaƙina,
kayan yaƙina,
da kai ne na ragargaza ƙasashe,
da kai ne na hallaka mulkoki,
21 da kai ne na ragargaza doki da mahayi,
da kai ne na ragargaza keken yaƙin da matuƙi,
22 da kai ne na ragargaza miji da mata,
da kai ne na ragargaza tsoho da saurayi,
da kai ne na ragargaza saurayi da budurwa,
23 da kai ne na ragargaza makiyayi da garke,
da kai ne na ragargaza manoma da dawakan noma,
da kai ne na ragargaza masu mulki da shugabanni.

24 “Zan sāka wa Babilon da dukan mazaunan Babilon a idanunku saboda dukan
muguntar da suka aikata a Sihiyona,” in ji Ubangiji.
25 “Ga shi, ina gāba da kai, ya ke dutse mai hallakarwa,
wadda ta hallaka duniya duka,”
in ji Ubangiji.
“Zan miƙa hannuna gāba da ke,
zan mirgina ƙasa daga ƙwanƙolin dutse,
zan maishe ki ƙonannen dutse.
26 Ba za a ɗauki dutsen yin kusurwa daga gare ki ba
ko na kafa harsashen gini,
gama za ki zama marar amfani har abada,” in ji Ubangiji.

27 “Ku tā da tuta a ƙasa!
Ku busa ƙahoni a cikin ƙasashe!
Ku shirya ƙasashe don yaƙi da ita,
ku kira waɗannan mulkokin gāba da ita.
Ararat, Minni, da Ashkenaz.
A naɗa shugaba gāba da ita;

ku shirya dawakai kamar fāra.
28 Ku shirya ƙasashe don yaƙi da ita,
sarakunan Medes,
gwamnoninsu da dukan masu shugabancinsu
da kowace ƙasar da take ƙarƙashin mulkinsu.
29 Kasa ta girgiza tana makyarkyata
saboda nufin UBANGIJI na gāba da Babilon ya tabbata,
nufinsa na mai da ƙasar Babilon kufai
don kada kowa yă zauna a can.
30 Sojojin Babilon sun daina yaƙi,
suna zaune a cikin kagaransu.
Karfinsu ya ƙare,
sun zama mata.
An sa wa wuraren zamanta wuta,
an karya ƙyamaren ƙofofin garinta.
31 Maguji yana biye da maguji a guje,
jakada yana biye da jakada,
don su faɗa wa sarkin Babilon,
cewa an ci birninsa a kowane gefe.
32 An ƙwace mashigai
aka ƙone fadamu da wuta,
sojoji kuma suka giggice."
33 Ni UBANGIJI Maɗaukaki, Allah na Isra'ila na ce,
"'Yar Babilon kamar daɓen masussuka
a lokacin da ake sussuka,
ba da daɗewa ba lokacin girbe ta zai zo."

34 "Nebukadnezzar sarkin Babilon ya cinye mu,
ya sa muka rikice,
ya maishe mu kamar tulun da babu kome a cikinsa.
Ya cinye mu kamar yadda dodon ruwa yakan yi
ya kuma cika cikinsa da kayan marmarinmu,
sa'an nan kuma ya yi amanmu.
35 Bari abin da aka yi wa jikinmu yă kasance a bisa Babilon,"
in ji mazaunan Sihiyona.
"Bari jininmu yă kasance a kan waɗanda suke zama a Babilon,"
in ji Urushalima.
36 Saboda haka ga abin da UBANGIJI ya ce,
"Duba, zan tsaya muku,
zan ɗaukar muku fansa,
zan sa tekunta kafe
in kuma sa maɓulɓulanta su ƙafe.
37 Babilon za tă zama tarin juji,
wurin zaman diloli,
abin ƙyama da abar ba'a,
inda ba kowa.
38 Mutanenta duk suna ruri kamar zakoki,
suna gurnani kamar 'ya'yan zaki.
39 Amma sa'ad da aka farkar da su,
zan yi musu biki
in sa su sha su bugu,
domin yi sowa da dariya,

sa'an nan su shiga barcin da ba za su farka ba,"
in ji UBANGIJI.
40 "Zan sauko da su
kamar tumaki zuwa mayanka,
kamar raguna da bunsurai.

41 "Yadda za a ci Sheshak,
taƙamar duniya duka za tă daina!
Babilon za tă zama abar ƙyama
a cikin al'ummai!
42 Teku zai malalo a kan Babilon,
raƙumansa masu hauka za su rufe ta.
43 Garuruwanta sun zama abin kufai,
za tă zama hamada inda ba ruwa,
ƙasar da ba mazauna,
ba kuma mutumin da zai ratsa ta cikinta.
44 Zan hukunta Bel a Babilon,
in sa ya yi aman abin da ya haɗiye.
Kasashe ba za su ƙara bumbuntowa wurinsa ba.
Katangan Babilon kuwa za tă rushe!

45 "Ku fito daga cikinta, jama'ata!
Ku tsere da ranku!
Ku tsere daga zafin fushin UBANGIJI.
46 Kada zuciyarku tă yi suwu ko ku ji tsoro
sa'ad da aka ji labarin a ƙasar,
labari guda a wannan shekara, wani kuma a ta biye,
labarin hargitsi a ƙasar
mai mulki ya tasar wa mai mulki.
47 Gama kwanaki tabbatacce suna zuwa,
sa'ad da zan hukunta gumakan Babilon,
zan kunyatar da dukan ƙasar
kuma matattunta duk za su kwanta a cikinta.
48 Sa'an nan sama da ƙasa da dukan abin da yake cikinsu,
za su yi sowa ta murna a kan Babilon,
gama daga arewa
masu hallakarwa su auko mata,"
in ji UBANGIJI.

49 "Babilon za tă fāɗi saboda kisassun mutanen Isra'ila,
kamar dai yadda kisassu dukan duniya
suka fāɗi saboda Babilon.
50 Ku waɗanda kuka tsere wa takobi,
ku gudu kada ku tsaya!
Ku tuna da UBANGIJI a ƙasa mai nesa,
ku kuma yi ta tunani a kan Urushalima."

51 "Mun sha kunya
saboda zargin da ake yi mana
kunya ta rufe mu,
domin baƙi sun shiga
tsarkakan wurare na gidan UBANGIJI."

52 “Amma kwanaki suna zuwa,” in ji UBANGIJI,
“sa’ad da zan hukunta gumakanta,
da kuma a dukan ƙasarta
waɗanda aka yi wa rauni, za su yi nishi.
53 Ko da Babilon za tă kai sararin sama ne,
ta gina kagaranta mai ƙarfi,
duk da haka zan aiki masu hallakarwa a kanta,”
in ji UBANGIJI.

54 “Ku ji muryar kuka daga Babilon,
Da hargowar babbar hallakarwa
daga ƙasar Babiloniyawa!
55 Gama UBANGIJI zai rushe Babilon,
zai sa ta ƙame bakinta na alfarma.
Sojoji za su yi ta kutsawa kamar raƙuman ruwa;
suna tā da muryoyinsu.
56 Gama mai hallakarwa ya auka wa Babilon,
a kama sojojinta,
a kuma kakkarya bakkunansu.
Gama UBANGIJI shi Allah ne mai sakayya;
zai yi sakayya sosai.
57 Zan sa mahukuntanta da masu hikimarta,
gwamnoninta, shugabanninta da sojojinta su sha su bugu;
za su dinga yin barcin da ba za su farka ba,”
in ji Sarkin, mai suna UBANGIJI Maɗaukaki.
58 Ni UBANGIJI Maɗaukaki, na ce,
“Za a baje katangan nan na Babilon mai kauri
za a kuma ƙone dogayen ƙyamarenta da wuta;
mutane sun wahalar da kansu a banza,
al’umma sun yi wahala kawai domin wutar lalata.”
59 Jawabin da annabi Irmiya ya ba Serahiya, ɗan Neriya, wato, jikan Ma’asehiya,
lokacin da ya tafi tare da Zedekiya, Sarkin Yahuda, zuwa Babilon a shekara ta huɗu
ta mulkinsa. Serahiya shi ne shugaba mai lura da gidajen saukar baƙi. 60 Irmiya
ya rubuta a littafi dukan masifun da za su auko wa Babilon, wato, dukan wannan
magana da aka rubuta a kan Babilon. 61 Irmiya kuwa ya ce wa Serahiya, “Lokacin
da ka kai Babilon, sai ka karanta dukan maganan nan. 62 Ka kuma ce, ‘Ya UBANGIJI,
kai ne ka yi magana a kan wannan wuri, cewa za ka lalatar da shi, har ba abin da
zai zauna a ciki, mutum ko dabba. Wurin zai zama kufai har abada.’ 63 Sa’ad da ka
gama karanta wannan littafi, sai ka ɗaura wa littafin dutse, sa’an nan ka jefar da shi
tsakiyar Kogin Yuferites. 64 Sa’an nan ka ce, ‘Haka Babilon za tă nutse, ba za tă ƙara
tashi ba saboda masifar da zan kawo mata. Mutanenta kuwa za su fāɗi.’ ”
Wannan shi ne ƙarshen kalmomin Irmiya.

# 52

*Fāɗuwar Urushalima*
*(2 Sarakuna 24.18–25.30; 2 Tarihi 36.11-21)*

1 Zedekiya yana da shekara ashirin da ɗaya sa’ad da ya ci sarauta. Ya yi mulki
a Urushalima shekara goma sha ɗaya. Sunan uwarsa Hamutal, ’yar Irmiya, wanda
yake zaune a Libna. 2 Sarki Zedekiya ya aikata abin da yake mugu a gaban UBANGIJI
kamar yadda Sarki Yehohiyakim ya yi. 3 Al’amarin ya zama da muni ƙwarai a cikin

Isra'ila da Yahuda, don haka UBANGIJI ya husata har ya sa aka kai mutanen bautar
talala.

Zedekiya kuwa ya tayar wa Sarkin Babilon.

4 A kan rana ta goma ga watan goma, a shekara ta tara ta mulkin Zedekiya, Sarkin
Yahuda, sai Nebukadnezzar, Sarkin Babilon, ya zo yaƙi da Urushalima tare da dukan
sojojinsa. Suka kewaye ta da yaƙi, suka gina katanga kewaye da ita. 5 An kewaye
birnin da yaƙi har shekara ta goma sha ɗaya ta mulkin Zedekiya.

6 A kan rana ta tara a watan huɗu na wannan shekara, yunwa ta tsananta ƙwarai
a birnin. Mutane suka rasa abin da za su ci. 7 Sai aka huda katangan birnin, sojojin
kuwa suka gudu, suka fita daga cikin birnin da dare ta hanyar ƙofar da take tsakanin
bango biyu, kusa da gonar sarki, sa'ad da Babiloniyawa suke kewaye da birnin.
Sojojin suka nufi wajen Araba. 8 Amma sojojin Babiloniyawa suka runtumi sarki
Zedekiya, suka ci masa a filayen Yeriko. Dukan sojoji suka yashe shi.

9 Da aka kama Zedekiya, sai aka kai shi wurin Sarkin Babilon a Ribla a ƙasar Hamat,
a nan ne Sarkin Babilon ya yanke masa shari'a. 10 Sarkin Babilon ya kashe 'ya'yan
Zedekiya a idonsa. Ya kuma kashe dukan shugabannin Yahuda a Ribla. 11 Sa'an nan
ya ƙwaƙule idanun Zedekiya, ya kuma sa masa ƙuƙumi, aka kai shi Babilon inda aka
sa shi a kurkuku har ran da ya mutu.

12 A kan rana ta goma ga watan biyar a shekara ta goma sha tara ta sarautar
Nebukadnezzar, Sarkin Babilon, sai Nebuzaradan shugaban matsara da kuma ɗan
majalisar sarki, ya zo Urushalima. 13 Sai ya ƙone haikalin UBANGIJI, da gidan sarki,
da dukan gine-gine masu alfarman da suke Urushalima. 14 Sojojin Babiloniyawa da
suke tare da shugaban matsara, suka rushe dukan katangan Urushalima. 15 Sa'an nan
Nebuzaradan shugaban matsara ya kwashe waɗansu matalauta, da sauran mutane
da aka bari a birnin, da waɗanda suka gudu zuwa wurin Sarkin Babilon, da sauran
masu sana'a, ya kai su bautar talala a Babilon. 16 Amma ya bar waɗansu matalauta
na gaske a ƙasar don su yi aiki a gonakin inabi, da sauran gonaki.

17 Babiloniyawa kuwa suka farfasa ginshiƙan tagulla, da dakalai, da babbar
kwatarniya, waɗanda suke a haikalin UBANGIJI. Suka kwashe tagulla duka suka kai
Babilon. 18 Suka kwashe tukwanen ƙarfe, da manyan cokula, da hantsuka, da daruna,
da tasoshin ƙona turare, da kayayyakin tagulla waɗanda ake amfani da su domin
hidimar haikali. 19 Suka kuma kwashe ƙananan kwanonin sha, da farantan wuta, da
daruna, da tukwane, da alkukai, da tasoshin ƙona turare, da kwanonin miƙa hadayar
sha. Duk abin da yake na zinariya da azurfa, shugaban matsara ya kwashe.

20 Tagullar da sarki Solomon ya yi wa haikalin UBANGIJI da ita, wato, ginshiƙai
biyu, da ƙaton kwano mai suna Teku na tagulla, da bijimai goma sha biyu, waɗanda
suke ɗauke da kwatarniya, da dakalai, ta fi ƙarfin a auna. 21 Tsawon kowane ginshiƙi
kamu goma sha takwas ne, kewayensa kuwa kamu goma sha biyu ne, kaurinsa kuma
huɗu ne. Kowannensu yana da rami a ciki. 22 A kan kowane ginshiƙi, an yi masa
dajiyar tagulla, tsayinta kamu biyar. A bisa kan kowace dajiya akwai raga da siffofin
rumman na tagulla kewaye da dajiyar. Ginshiƙi na biyu ma haka yake da siffofin
rumman. 23 Akwai siffofin rumman tasa'in da shida da ake gani a gefen. Dukan
siffofin rumman da suke a kan ragar kewaye, guda ɗari ne.

24 Shugaban matsara kuma ya ɗauki Serahiya babban firist, da Zefaniya wanda
yake biye da babban firist, da mutum uku masu tsaron ƙofar, ya tafi da su. 25 Daga
cikin birnin kuma ya ɗauki shugaban sojojin, da mutum bakwai 'yan majalisar sarki,
da magatakardan shugaban sojojin wanda yakan tara sojojin ƙasar, da mutane sittin
na ƙasar, waɗanda aka same su a birnin, ya tafi da su. 26 Nebuzaradan shugaban
matsara ya tafi da waɗannan mutane wurin Sarkin Babilon a Ribla, 27 Sarkin Babilon
kuwa ya kashe su a Ribla a ƙasar Hamat.

Haka aka tafi da mutanen Yahuda bautar talala, daga ƙasarta.

28 Wannan shi ne yawan mutanen da Nebukadnezzar ya kai su bauta.

A shekara ta bakwai ta sarautarsa, ya tafi da Yahudawa 3,023;
29 a shekara ta goma sha takwas ta sarautar Nebukadnezzar,
ya tafi da Yahudawa daga Urushalima 832;
30 a shekara ta ashirin da uku ta sarautarsa,
Nebuzaradan shugaban matsara ya tafi da Yahudawa 745.

Jimillarsu duka 4,600 ne.

### *An saki Yehohiyacin*
### *(2 Sarakuna 25.27-30)*

31 A shekarar da Ewil-Merodak ya zama Sarkin Babilon, sai ya nuna wa Yehohiyacin
Sarkin Yahuda alheri. Ya fisshe shi daga kurkuku. Wannan ya faru ran ashirin
da biyar ga watan goma sha biyu a shekara ta talatin da bakwai bayan da aka kai
Yehohiyacin bauta. 32 Ewil-Merodak ya nuna wa Yehohiyacin alheri, ya ba shi matsayi
na daraja fiye da waɗansu sarakunan da aka kai su bautar talala a Babilon tare da shi.
33 Yehohiyacin ya tuɓe tufafin kurkuku, ya riƙa cin abinci kullum a teburin sarki, har
dukan sauran kwanakin ransa. 34 Kowace rana akan ba shi kyauta bisa ga umarnin
sarkin Babilon, saboda bukatarsa. Haka aka yi masa har rasuwarsa.

# Makoki

## 1

* 1 Yanzu birnin ya zama babu kowa a ciki,
birnin da a dā yake cike da mutane!
Yanzu birnin ya zama kamar gwauruwa,
wadda a dā babba ce ita a cikin ƙasashe!
Ita da take sarauniya a cikin larduna
yanzu ta zama baiwa.

2 Tana yin kuka mai zafi da dare,
hawaye na gangara a kan kumatunta.
A cikin masoyanta duka
babu wanda ya yi mata ta'aziyya.
Duk abokanta sun yashe ta;
sun zama abokan gābanta.

3 Bayan wahala da baƙin ciki,
Yahuda ta tafi bauta.
Ta zauna a cikin ƙasashe,
ba tă samu wurin hutawa ba.
Duk masu fafararta sun same ta
sa'ad da take cikin matuƙar ɓacin rai.

4 Hanyoyin zuwa Sihiyona suna makoki,
gama ba wanda ya zo bikin da ta shirya.
Ba kowa a hanyoyin shiganta.
Firistocinta suna gurnani,
'yan matana kuma suna wahala,
kuma tana cikin shan wahala ƙwarai.

5 Maƙiyanta sun zama shugabanninta;
Abokan gābanta suna da kwanciyar rai.
Ubangiji ya kawo mata ɓacin rai
domin yawan zunubanta.
'Ya'yanta sun tafi bauta,
a ƙarƙashin maƙiyanta.

6 Diyar Sihiyona ba ta
da sauran daraja.
'Ya'yan sarakunanta sun zama kamar bareyi
waɗanda suka rasa wurin kiwo;
cikin rashin ƙarfi suka guje
wa masu fafararsu.

7 A cikin kwanakin da take shan wahala take kuma yawo
Urushalima ta tuna da dukan dukiyar
da take da ita a kwanakin dā can.
Sa'ad da mutanenta suka faɗa cikin hannun abokan gābanta,

* 1: Wannan surar waƙa ce mai bin harufa bi da bi, ayoyin da suka fara da harufan Ibraniyanci bi da bi.

ba wanda ya taimake ta.
Maƙiyanta suka dube ta
suka yi mata dariya don hallakar da ta auko mata.

8 Urushalima ta yi zunubi ƙwarai
saboda haka ta zama marar tsarki.
Dukan masu martaba ta sun raina ta,
gama sun ga tsiraicinta;
ita ma da kanta tana nishi da ƙyar
ta kuma juya baya.

9 Kazantarta ta manne wa rigunanta;
ba tă kula da nan gaba ba,
fāɗuwarta kuwa babban abu ne;
babu wanda zai yi mata ta'aziyya.
"Duba, ya UBANGIJI, ka ga wahalata,
gama maƙiyi ya yi nasara."

10 Maƙiya ya kwashe
dukiyarta duka;
ta ga mutanen da ba su san Allah ba
sun shiga wuri mai tsarkinta
waɗanda ka hana su
shiga taron jama'arka.

11 Dukan mutanenta suna nishi
da ƙyar suna neman burodi;
sun sayar da dukiyarsu don su samu abinci
don kada su mutu da yunwa.
"UBANGIJI, ka duba ka gani,
gama an yashe ni."

12 "Ko wannan ba wani abu ba ne a wurinku, dukanku masu wucewa?
Ku duba ku gani.
Ko akwai wata wahala kamar
irin wadda nake sha,
wadda UBANGIJI ya auko mini
a cikin zafin fushinsa?

13 "Daga sama ya aiko da wuta,
ya aiko ta cikin ƙasusuwana.
Ya shimfiɗa raga a ƙafafuna
ya juyo da ni.
Ya bar ni ni kaɗai,
sumamme dukan yini.

14 "Ya ɗaura zunubaina a wuyana;
aka naɗe su a hannuwansa.
Aka rataye su a wuyana
Ubangiji ya kwashe ƙarfina.
Ya bashe ni
ga waɗanda suka fi ni ƙarfi.

15 “Ubangiji ya ƙi
duk mayaƙan da suke tare da ni;
ya sa wata runduna ta tayar mini
ta kuma tattake samarina.
Ubangiji ya tattake budurwa Diyar Yahuda
kamar ’ya’yan inabi a wurin matsewa.

16 “Dalilin da ya sa nake kuka ke nan
idanuna kuma suna ta zubar da hawaye.
Babu wani a kusa da zai yi mini ta’aziyya,
ba wanda zai sabunta ruhuna.
’Ya’yana sun zama fakirai
domin maƙiyina ya yi nasara.”

17 Sihiyona ta miƙa hannunta,
amma ba wani da zai yi mata ta’aziyya.
Ubangiji ya umarta cewa
maƙwabtansa za su zama maƙiyansa;
Urushalima ta zama
abar ƙyama a cikinsu.

18 “Ubangiji mai adalci ne,
duk da haka na yi tawaye da umarninsa.
Ku saurara, jama’a duka;
ku dubi wahalar da nake sha.
Samarina da ’yan matana
duka sun tafi bauta.

19 “Na kira abokaina
amma sun yashe ni.
Firistocina da dattawana
sun hallaka a cikin birnin
yayinda suke neman abinci
don kada su mutu da yunwa.

20 “Duba, Ubangiji, ka ga ƙuncin da nake ciki!
Ina shan azaba a raina,
ba ni da kwanciyar rai a cikin zuciyata,
domin na yi tawaye sosai.
A waje takobi na kisa;
a ciki kuma akwai mutuwa.

21 “Mutane suna ji ina nishi da ƙyar,
amma ba wanda zai yi mini ta’aziyya.
Dukan maƙiyana sun ji wahalar da nake ciki;
suna farin ciki da abin da ka yi.
Ka kawo ranan nan da ka sanar
domin su ma su zama kamar ni.

22 “Bari ka ga muguntarsu duka;
ka yi musu
yadda ka yi mini
domin dukan zunubansu.

Nishina da yawa
kuma zuciyata ta gaji.”

## 2

* 1 Yadda Ubangiji ya rufe Diyar Sihiyona
da gizagizan fushi!†
Ya jefar da darajar Isra’ila
daga sama zuwa ƙasa;
bai tuna da wurin ɗora ƙafafunsa ba
a ranar fushinsa.

2 Ubangiji ya hallakar
da wurin zaman Yaƙub ba tausayi;
A cikin fushinsa kuma zai rurrushe
kagaran Diyar Yahuda.
Ya ƙasƙantar da mulki
da masu mulki.

3 A cikin zafin fushi ya fasa
kowane ƙaho na Isra’ila.
Ya janye hannun damansa
sa’ad da maƙiyi ya zo.
Ya yi ƙuna a cikin Yaƙub kamar wuta mai ƙone
duk abin da yake kusa da ita.

4 Kamar abokin gāba, ya ɗana bakansa;
hannun damansa na shirye.
Kamar maƙiyi,
ya kashe duk wanda idonsa ya ji daɗin gani;
ya zuba fushinsa kamar wuta
a kan tenti na Diyar Sihiyona.

5 Ubangiji kamar maƙiyi ne;
ya hallaka Isra’ila.
Ya hallaka wurarenta duka
ya kuma hallaka kagaranta.
Ya ƙara yawan makoki da baƙin ciki
wa Diyar Yahuda.

6 Ya rushe haikalinsa kamar lambu;
ya hallaka wurin yi masa sujada.
UBANGIJI ya sa Sihiyona ta manta
da bukukkuwanta da kuma ranakunta na Asabbaci;
a cikin zafin fushinsa
ya watsar da sarki da firist.

7 Ubangiji ya ƙi bagadensa
ya kuma yi wofi da haikalinsa.

---

* **2:** Wannan surar waƙa ce mai bin harufa bi da bi, ayoyin da suka fara da harufan Ibraniyanci bi da bi. † **2:1** Ko kuwa Yadda UBANGIJI cikin fushinsa / ya yi da Diyar Sihiyona da wargi

Ya ba maƙiyinta fadodinta;
suka yi sowa a cikin gidan UBANGIJI
kamar a ranar da ake yin biki.

8 UBANGIJI ya ƙuduri niyya yǎ rushe bangon
da yake kewaye da Diyar Sihiyona.
Ya auna da igiyar awo
bai fasa hallaka ta ba.
Ya sa katanga da katanga
duk suka lalace.

9 Kofofinta sun nutse a cikin ƙasa;
ya kakkarya ƙarafanta.
Sarakunanta da ʼyaʼyan sarakunanta
duk an kai su bauta cikin waɗansu ƙasashe,
babu sauran doka,
annabawa kuma ba su samun
wahayi daga wurin UBANGIJI.

10 Dattawan Diyar Sihiyona
sun zauna shiru a ƙasa;
suka kuma sa rigar buhu.
ʼYan matan Urushalima suka
sunkuyar da kawunansu ƙasa.

11 Idanuna sun dushe don yawan kuka,
raina na cike da baƙin ciki;
zuciyata ta karaya
domin mutanena sun hallaka,
domin yara da jarirai suna suma
a kan hanyoyi a cikin birni.

12 Suna ce wa uwayensu,
"Ina burodi da ruwan inabi?"
Yayinda suke suma kamar mutanen
da aka ji masu ciwo a cikin birni,
saʼad da suke mutuwa
a hannuwan uwayensu.

13 Me zan ce miki?
Da me zan kwatanta ki,
ke Diyar Urushalima?
Da me zan misalta ki,
yadda zan iya yi miki taʼaziyya,
Ke Budurwa Diyar Sihiyona?
Ciwonki yana da zurfi kamar teku.
Wane ne zai iya warkar da ke?

14 Wahayin annabawanki
ƙarya ne kuma marasa amfani;
ba su tona zunubanki ba
yadda za su iya ceto ki daga bauta ba.
Sun yi miki annabcin ƙarya

marar amfani.

15 Duk masu wucewa
suna yi miki tafi na reni;
suna yi wa Diyar Urushalima
tsaki suna kaɗa kai suna cewa,
“Wannan ne birnin da aka ce
kyakkyawa ne,
mai farantawa dukan duniya rai?”

16 Maƙiyanki duka suna ta surutu
game da ke;
suna tsaki suna cizon haƙora
suna cewa, “Mun hallaka ta.
Wannan ce ranar da muke jira;
yau mun gan ta.”

17 UBANGIJI ya yi abin da ya shirya;
ya cika maganarsa,
wadda ya umarta tun daɗewa.
Ya jefar da ke ba tausayi,
ya bari maƙiya sun yi nasara da ke,
ya ɗaukaka ƙahon maƙiyanki.

18 Zuciyar mutane
ta yi kuka ga UBANGIJI.
Ya bangon Diyar Urushalima,
bar hawayenki su zuba kamar rafi
dare da rana;
kada ki huta,
kada idanunki su huta.

19 Ki tashi, ki yi kuka cikin dare,
dare na yi sai ki fara kuka;
kina buɗewa Ubangiji zuciyarki.
Ki ɗaga hannuwanki gare shi
domin rayukan ’ya’yanki,
waɗanda suka suma don yunwa
a kan kowane titi.

20 “Ka duba, ka gani ya UBANGIJI.
Wane ne ka taɓa yi wa haka?
Ko ya kamata uwaye su ci ’ya’yansu,
’ya’yan da suka yi reno?
Ko ya kamata a kashe firistoci da annabawa
a cikin haikalin Ubangiji?

21 “Matasa da tsofaffi duk
suna kwanciya a cikin ƙurar tituna;
an karkashe matasa
da ’yan matana da takobi.
Ka kashe su a ranar fushinka;

ka kashe su ba tausayi.

22 “Kamar yadda kake yin gayyata a ranar biki,
haka kake kawo mini tsoro a kowane gefe.
A ranar fushin UBANGIJI
ba mai tserewa ba wanda zai tsira;
maƙiyina ya kashe waɗanda na yi renonsu,
na kuma lura da su.”

# 3

* 1 Ni ne mutumin da ya ga azaba
ta wurin bulalar fushin UBANGIJI.
2 Ya kore ni, ya sa na yi tafiya
a cikin duhu maimakon a cikin haske;
3 ba shakka, ya juya mini baya, yana gāba da ni
sau da sau, dukan yini.

4 Ya sa fatar jikina da naman jikina sun tsufa
ya kuma karya ƙasusuwana.
5 Ya yi mini kwanton ɓauna ya kuma kewaye ni
da baƙin ciki da kuma wahala.
6 Ya sa na zauna a cikin duhu
kamar waɗanda suka mutu da jimawa.

7 Ya kewaye ni yadda ba zan iya gudu ba;
Ya daure ni da sarƙa mai nauyi.
8 Ko lokacin da nake kira don neman taimako,
ba ya jin addu’ata.
9 Ya tare hanyata da tubula na duwatsu;
ya sa hanyata ta karkace.

10 Kamar beyar da take a laɓe tana jira,
kamar zaki a ɓoye,
11 ya janye ni daga kan hanya ya ɓatar da ni
ya bar ni ba taimako.
12 Ya ja kwarinsa
ya sa in zama abin baratarsa.

13 Ya harbi zuciyata
da kibiyoyin kwarinsa.
14 Na zama abin dariya ga mutanena duka;
suna yi mini ba’a cikin waƙa dukan yini.
15 Ya cika ni da kayan ɗaci
ya gundure ni da abinci mai ɗaci.

16 Ya kakkarya haƙorana da tsakuwa;
ya tattake ni cikin ƙura.

* **3:** Wannan surar waƙa ce; ayoyin kowane sakin layi sun fara da harufan Ibraniyanci bi da bi, kuma ayoyin cikin kowane sakin layi ya fara da harufa iri ɗaya.

17 An hana ni salama;
na manta da ko mene ne ake kira wadata.
18 Saboda haka na ce, “Darajata ta ƙare
da kuma duk abin da nake begen samu daga wurin UBANGIJI.”

19 Na tuna da azabata da kuma sintiri,
da na yi ta yi da ɗacin rai.
20 Na tuna su sosai,
sai kuma na ji ba daɗi a raina.
21 Duk da haka na tuna da wannan
na kuma sa bege ga nan gaba.

22 Domin ƙaunar UBANGIJI ba mu hallaka ba;
gama jiyejiyanƙansa ba su ƙarewa.
23 Sababbi ne kowace safiya;
amincinka kuwa mai girma ne.
24 Na ce wa kaina, “UBANGIJI shi ne nawa;
saboda haka zan jira shi.”

25 UBANGIJI mai alheri ne ga waɗanda suke da bege a cikinsa,
ga kuma wanda yake neman shi;
26 yana da kyau ka jira shiru
domin samun ceton UBANGIJI.
27 Yana da kyau mutum yă sha wuya
tun yana yaro.

28 Bari yă zauna shiru shi kaɗai,
gama haka UBANGIJI ya sa yă yi.
29 Bari yă ɓoye fuskarsa cikin ƙura
kila akwai bege.
30 Bari yă ba da kumatunsa a mare shi,
yă kuma bari a ci masa mutunci.

31 Gama Ubangiji ba ya
yashe mutane har abada.
32 Ko da ya kawo ɓacin rai, zai nuna tausayi sosai,
ƙaunarsa tana da yawa.
33 Gama ba haka kawai yake kawo wahala
ko ɓacin rai ga ’yan adam ba.

34 Bai yarda a tattake
’yan kurkuku a ƙasa ba,
35 ko kuma a danne wa mutum hakkinsa
a gaban Maɗaukaki,
36 ko kuma a danne wa mutum shari’ar gaskiya
ashe Ubangiji ba zai ga irin waɗannan abubuwa ba?

37 Wane ne ya isa yă yi magana kuma ta cika
in ba Ubangiji ne ya umarta ba?
38 Ba daga bakin Maɗaukaki ne
bala’i da abubuwa masu kyau suke fitowa ba?

39 Don mene ne wani mai rai zai yi gunaguni
sa'ad da aka ba shi horo domin zunubansa?

40 Bari mu auna tafiyarmu mu gwada ta,
sai mu kuma koma ga UBANGIJI.
41 Bari mu ɗaga zuciyarmu da hannuwanmu
ga Allah na cikin sama, mu ce,
42 "Mun yi zunubi mun yi tawaye
ba ka kuwa gafarta ba.

43 "Ka rufe kanka da fushi, ka fafare mu;
ka karkashe mu ba tausayi.
44 Ka rufe kanka da gajimare
don kada addu'armu ta kai wurinka.
45 Ka mai da mu tarkace da juji
a cikin mutane.

46 "Dukan maƙiyanmu suna ta yin mana magana
marar daɗi.
47 Muna cika da tsoro,
da lalatarwa da hallakarwa."
48 Hawaye na kwararowa daga idanuna
domin an hallaka mutanena.

49 Idanuna za su ci gaba da kwararowa da hawaye,
ba hutawa.
50 Har sai in UBANGIJI ya duba
daga sama ya gani.
51 Abin da nake gani yana kawo mini baƙin ciki
domin dukan matan birnina.

52 Maƙiyana suna farauta ta
ba dalili kamar tsuntsu.
53 Sun yi ƙoƙari su kashe ni a cikin rami
suka kuma jajjefe ni da duwatsu;
54 ruwaye suka rufe kaina,
sai na yi tunani cewa na kusa mutuwa.

55 Na yi kira ga sunanka, ya UBANGIJI,
daga rami mai zurfi.
56 Ka ji roƙona, "Kada ka toshe kunnuwanka
ka ƙi jin roƙona na neman taimako."
57 Ka zo kusa lokacin da na kira ka,
kuma ka ce mini, "Kada ka ji tsoro."

58 Ya Ubangiji, ka goyi bayana;
ka fanshi raina.
59 Ya UBANGIJI, ka ga inda aka yi mini ba daidai ba.
Ka shari'anta, ka ba ni gaskiya!
60 Ka ga zurfin ramakonsu,
da duk mugun shirin da suke yi mini.

61 Ya Ubangiji, ka ji zaginsu,
da duka mugun shirin da suke yi mini
62 Abin da maƙiyana suke yin raɗa a kai
game da ni duk yini.
63 Dube su! A zaune ko a tsaye,
suna yi mini ba'a cikin waƙoƙinsu.

64 Ka ba su abin da ya dace su samu, ya Ubangiji,
domin abin da hannuwansu suka yi.
65 Ka sa yana ta rufe zuciyarsu,
kuma bari la'anarka ta bi su.
66 Ka fafare su cikin fushi
ka hallaka su daga cikin duniya ta Ubangiji.

# 4

* 1 Zinariya ta rasa kyanta,
hasken zinariya ya dushe!
An warwatsar da tsarkakakkun duwatsu
masu daraja a kan krituna.

2 Dubi samarin Sihiyona masu daraja,
waɗanda a dā darajarsu ta isa nauyin zinariya,
yanzu ana ɗaukar su a matsayin tukwanen ƙasa,
aikin maginin tukwane!

3 Ko diloli suna ba 'ya'yansu nono su sha,
amma mutanena sun zama marasa zuciya
kamar jiminai a cikin jeji.

4 Domin ƙishirwa
harshen jarirai ya manne a rufin bakinsu;
yaran suna roƙo a ba su burodi,
amma ba wanda ya ba su.

5 Waɗanda a dā sukan ci abinci mai daɗi
yanzu su ne masu bara a tituna.
Waɗanda a dā suke sa kaya masu kyau
yanzu suna kwance a kan tarin toka.

6 Horon mutanena
ya fi na Sodom girma,
wadda aka hallaka farat ɗaya
ba wani hannu da ya juya ya taimake ta.

7 'Ya'yan sarakunansu sun fi ƙanƙara haske
sun kuma fi madara fari,
jikunansu sun fi murjani ja,
kyansu kamar shuɗin yakutu.†

* **4:** Wannan surar waƙa ce mai bin harufa bi da bi, ayoyin da suka fara da harufan Ibraniyanci bi da bi. † **4:7** Ko kuma lafis lazuli

8 Amma yanzu sun fi dare duhu;
ba a iya gane su a tituna.
Fatar jikinsu ta manne da ƙasusuwansu;
sun bushe kamar itace.

9 Gara waɗanda aka kashe su da takobi
da waɗanda suke mutuwa da yunwa;
sun rame domin rashin abinci a gona.

10 Da hannuwansu mata masu tausayi
sun dafa yaransu,
suka zama masu abinci
sa'ad da aka hallaka mutanena.

11 UBANGIJI ya saki fushinsa;
ya zuba zafin fushinsa.
Ya hura wuta a Sihiyona
ta kuma cinye harsashin gininta.

12 Sarakunan duniya ba su gaskata ba,
haka ma mutanen duniya,
cewa magabta da maƙiya
za su iya shiga ƙofofin Urushalima.

13 Amma ya faru domin zunuban annabawanta
da muguntar firistocinta,
waɗanda suka zub
da jinin masu adalci a cikinsu.

14 Yanzu suna yawo barkatai a tituna
kamar makafi.
Sun ƙazantu da jini
yadda ba wanda zai kuskura ya taɓa rigunansu.

15 "Ku tafi! Ba ku da tsabta!" Haka mutane suke ihu suke ce musu.
"Ku tashi daga nan! Ku tashi daga nan! Kada ku taɓa mu!"
Sa'ad da suka gudu suna yawo,
mutanen waɗansu ƙasashe suka ce,
"Ba za su ci gaba da zama a nan ba."

16 UBANGIJI kansa ya warwatsa su;
ya daina duban su.
Ba a ba firistoci girma,
ba su ba dattawa gata.

17 Idanunmu sun gaji,
suna ta dubawa ko taimako zai zo;
mu sa ido ko za mu ga
ƙasar da za tă iya taimakon mu.

18 Ana bin sawunmu,
ba za mu iya tafiya kan tituna ba.

Karshenmu ya kusa, kwanakinmu sun ƙare,
gama ƙarshenmu ya zo.

19 Masu fafarar mu sun fi gaggafa
mai firiya a sararin sama sauri;
sun fafare mu a kan duwatsu
suna fakon mu a jeji.

20 Shafaffe na UBANGIJI, numfashin ranmu,
ya fāɗi cikin tarkonsu.
Muna tunani cewa za mu iya rayuwa
cikin sauran mutane a ƙarƙashin inuwarsa.

21 Ku yi murna da farin ciki, ya Diyar Edom,
ke mai zama a ƙasar Uz.
Amma ke ma za a ba ki kwaf;
za ki bugu ki zama tsirara.

22 Ya Diyar Sihiyona, hukuncinki zai ƙare;
ba zai sa zaman bautarki yă yi tsayi ba.
Amma ya Diyar Edom, zai hukunta zunubinki
yă tona tsiraicinki.

# 5

1 Ka tuna, ya UBANGIJI, abin da ya faru da mu;
duba, ka ga kunyar da muka sha.
2 An ba wa baƙi gādonmu,
gidajenmu kuma aka ba bare.
3 Mun zama marayu marasa ubanni,
uwayenmu kamar gwauraye.
4 Dole mu sayi ruwan da muke sha;
sai mun biya mu sami itace.
5 Masu fafararmu sun kusa kama mu;
mun gaji kuma ba dama mu huta.
6 Mun miƙa kanmu ga Masar da Assuriya
don mu sami isashen abinci.
7 Kakanninmu sun yi zunubi
kuma ba sa nan yanzu,
mu ne aka bari muna shan hukuncinsu.
8 Bayi suna mulki a kanmu,
kuma ba wanda zai ʼyantar da mu daga hannuwansu.
9 Muna samun burodi a bakin rayukanmu
domin takobin da yake a jeji.
10 Fatar jikinmu ta yi zafi kamar murhu,
muna jin zazzaɓi domin yunwa.
11 An yi wa mata fyaɗe a cikin Sihiyona,
da kuma budurwai a cikin garuruwan Yahuda.
12 An rataye ʼyaʼyan sarakuna da hannuwansu;
ba a ba wa dattawa girma.
13 Samari suna faman yin niƙa;

yara kuma suna fama da ƙyar da nauyin kayan itace.
14 Dattawan sun bar ƙofar birnin,
samari sun daina rera waƙa.
15 Farin ciki ya rabu da zuciyarmu;
rayuwarmu ta zama makoki.
16 Rawani ya fāɗi daga kanmu.
Kaiton mu gama mun yi zunubi!
17 Domin wannan zuciyarmu ta yi sanyi;
domin waɗannan abubuwa idanunmu sun dushe
18 gama Tudun Sihiyona ya zama kufai,
sai diloli ke yawo a wurin.

19 Ya UBANGIJI, kai ne mai iko har abada;
kursiyinka ya dawwama cikin dukan zamani.
20 Don mene ne kake mantawa da mu koyaushe?
Me ya sa ka yashe mu da jimawa?
21 Ka sāke jawo mu gare ka, ya UBANGIJI, don mu komo;
ka sabunta kwanakinmu su zama kamar yadda suke a dā
22 sai dai in ka ƙi mu gaba ɗaya
kana fushi da mu fiye da yadda za a iya aunawa.

# Ezekiyel

### *Halittu masu rai da kuma ɗaukakar UBANGIJI*

1 A[*] shekara ta talatin, a wata na huɗu a rana biyar, yayinda nake cikin ʼyan zaman
bauta kusa da Kogin Kebar, sai sammai suka buɗe na kuwa ga wahayoyin Allah.
2 A rana biyar ga wata, a shekara ta biyar ne ta zaman bautan Sarki Yehohiyacin,
3 maganar UBANGIJI ta zo wa Ezekiyel firist, ɗan Buzi,[†] kusa da Kogin Kebar a ƙasar
Babiloniyawa.[‡] A can hannun UBANGIJI yana a kansa.
4 Na duba, sai na ga guguwa ta taso daga arewa babban hadari cike da walƙiya
kewaye da haske mai haske sosai. Tsakiyar wutar ta yi kamar ƙarfe mai cin wuta
balbal, 5 a cikin wutar kuwa akwai abin da ya yi kamar halittu guda huɗu. A bayyane
kamanninsu ya yi kamar siffar mutum, 6 amma kowannensu yana da fuskoki huɗu
da fikafikai guda huɗu. 7 Kafafunsu miƙaƙƙu ne; kuma ƙafafunsu sun yi kamar na
maraƙi suna kuma walƙiya kamar tagullar da aka goge. 8 A ƙarƙashin fikafikansu
huɗu suna da hannuwan mutum a kowane gefe. Dukansu huɗu suna da fuskoki da
fikafikai, 9 kuma fikafikansu suna taɓan juna. Kowanne ya miƙe gaba; ba sa juyawa
saʼad da suke tafiya.
10 Fuskokinsu sun yi kamar haka. Kowanne a cikin huɗun yana da fuskar
mutum, kuma a gefen dama kowanne yana da fuskar zaki, a hagu kuma fuskar
maraƙi; kowanne yana kuma da fuskar gaggafa. 11 Haka fuskokinsu suka kasance.
Fikafikansu sun buɗu sama; kowanne yana da fikafikai biyu, ɗaya yana taɓa fikafikan
ɗayan halittar a ɗayan gefe, fikafikai biyu kuma suna rufe jikinsa. 12 Kowanne ya
miƙe gaba sosai. Duk inda ruhu zai tafi, can za su, ba tare da juyawa ba yayinda suke
tafiya. 13 Kamannin halittun ya yi kamar garwashi mai cin wuta ko kuwa kamar fitilu.
Wuta tana kai da kawowa a cikin halittun; ta yi haske ƙwarai, walƙiya kuma tana
wulgawa daga cikinta. 14 Halittun suna gaggauta kai da kawowa kamar walƙiya.
15 Yayinda nake kallon rayayyun halittun nan, sai na ga daʼira a ƙasa kusa da
kowace halitta da fuskokinsa huɗu. 16 Ga kamanni da fasalin daʼirorin. Suna
ƙyalƙyali kamar kirisolit, kuma dukan huɗun sun yi kama da juna. Kowacce ta yi
kamar daʼira a cikin daʼira. 17 Yayinda suke tafiya, sukan nufi duk wani gefe guda
cikin gefe huɗun da halittun suka nufa; daʼirorin ba za su juya ba saʼad da halittun
suke tafiya. 18 Karafansu da suka yi kamar zobe sun yi tsayi suna kuma da bantsoro,
dukan ƙarafan nan huɗu kuwa da suka yi kamar zobe suna cike da idanu a kewaye.
19 Saʼad da rayayyun halittun suke tafiya, daʼirorin da suke kusa da su kan motsa;
kuma saʼad da rayayyun halittun sun tashi sama, daʼirorin su ma sukan tashi sama.
20 Duk inda ruhu za shi, su ma can za su, kuma daʼirorin za su tashi tare da su, domin
ruhun rayayyun halittun nan yana a cikin daʼirorin. 21 Saʼad da halittun sun motsa,
sai su ma su motsa; saʼad da halittun sun tsaya cik, su ma sai su tsaya cik, saʼad
da kuma halittun sukan tashi sama, daʼirorin suka tashi tare da su, domin ruhun
rayayyun halittun nan yana a cikin daʼirorin.
22 A bisa kawunan rayayyun halittun nan akwai abin da ya yi kamar ƙanƙara,
mai bantsoro. 23 A ƙarƙashin alʼarshin fikafikansu sun miƙe kyam ɗaura da juna,
kuma kowanne yana da fikafikai biyu da suka rufe jikinsa. 24 Saʼad da halittun suke
tafiya, sai na ji ƙarar fikafikansu, kamar rurin ruwaye masu gudu, kamar muryar

* **1:1** Ko kuwa nawa † **1:3** Ko kuwa Ezekiyel ɗan Buzi firist ‡ **1:3** Ko kuwa Kaldiyawa

Maɗaukaki,§ kamar hayaniyar rundunar mayaƙa. In sun tsaya cik, sukan sauko da
fikafikansu.
25 Sai aka ji murya daga al'arshi a kan kawunansu yayinda suke tsaye da fikafikansu
a sauke. 26 A bisa al'arshin a kan kawunansu akwai abin da ya yi kamar saffaya,*
kuma a can bisa a kan kursiyin akwai siffa kamar na mutum. 27 Na ga daga abin da
ya yi kamar kwankwasonsa zuwa bisa ya yi kamar ƙarfe mai walƙiya, sai ka ce wuta,
kuma daga kwankwasonsa zuwa ƙasa ya yi kamar wuta; haske kuma mai walƙiya
sosai kewaye da shi. 28 Kamar kamannin bakan gizo a cikin gizagizai a ranar da aka
yi ruwan sama, haka hasken da ya kewaye shi.
Wannan shi ne kwatancin kamannin ɗaukakar UBANGIJI. Sa'ad da na gani, sai na
fāɗi rubda ciki, na kuma ji muryar wani tana magana.

# 2

*Kiran Ezekiyel*

1 Ya ce mini, "Ɗan mutum, tashi ka tsaya a ƙafafunka zan kuma yi maka magana."
2 Yayinda yake magana, sai Ruhu ya sauko mini ya kuma tā da ni a ƙafafuna, na
kuma ji shi yana mini magana.
3 Ya ce, "Ɗan mutum, ina aikan ka zuwa ga Isra'ilawa, zuwa ga al'ummar 'yan
tawayen nan da suka yi mini tayarwa; su da kakanninsu sun yi mini tawaye har yǎ
zuwa yau. 4 Mutanen da nake aikan ka masu ƙin ji ne da kuma taurinkai. Ka faɗa
musu cewa, 'Ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka ya faɗa.' 5 Kuma ko su ji ko kada su
ji, gama su gida ne mai tawaye, za su san cewa akwai annabi a cikinsu. 6 Kai kuwa,
ɗan mutum, kada ka ji tsoro, ko da sarƙaƙƙiya da ƙayayyuwa duk sun kewaye ka
kana kuma zama a cikin kunamai. Kada ka ji tsoron abin da za ka faɗa ko ka firgita
ta wurinsu, ko da yake su gida ne mai tawaye. 7 Dole ka yi maganata gare su, ko su
ji ko kada su ji, gama su 'yan tawaye ne. 8 Amma kai, ɗan mutum, ka saurari abin
da zan faɗa maka. Kada ka yi tawaye kamar wannan gidan 'yan tawaye; ka buɗe
bakinka ka kuma ci abin da na ba ka."
9 Sai na duba, na kuma ga hannu ya miƙe zuwa wurina. A cikinsa akwai littafi,
10 wanda ya nannaɗe a gabana. A kowane gefensa akwai rubutun kalmomin makoki
da kuka da kuma kaito.

# 3

1 Ya kuma ce mini, "Ɗan mutum, ka ci abin da yake a gabanka, ka ci wannan littafi;
sa'an nan ka tafi ka yi magana wa gidan Isra'ila." 2 Saboda haka na buɗe bakina, ya
kuma ba ni littafin in ci.
3 Sai ya ce mini, "Ɗan mutum, ka ci wannan littafin da nake ba ka, ka kuma cika
cikinka da shi." Sai na ci shi, ya kuma yi zaki kamar zuma a bakina.
4 Sa'an nan ya ce mini, "Ɗan mutum, yanzu ka tafi gidan Isra'ila ka faɗa kalmomina
gare su. 5 Ba ina aikan ka wurin mutanen da suke da baƙon harshe da kuma yare
mai wuya ba ne, amma zuwa ga gidan Isra'ila ne, 6 ba ga mutane da yawa na baƙon
harshe da yare mai wuya, waɗanda ba ka san kalmominsu ba. Tabbatacce da na aike
ka wurin irinsu, da sun saurare ka. 7 Amma gidan Isra'ila ba sa niyya su saurare ka
domin ba sa niyya su saurare ni, gama dukan gidan Isra'ila sun taurare suna kuma
kin ji. 8 Amma zan sa ka zama mai taurinkai da taurin zuciya kamar su. 9 Zan sa
goshinka ya zama da tauri kamar dutse, da tauri fiye da dutsen ƙanƙara ƙarfi. Kada
ka ji tsoronsu ko ka firgita ta wurinsu, ko da yake su gidan 'yan tawaye ne."
10 Ya kuma ce mini, "Ɗan mutum, ka ji da kyau ka kuma lura da dukan kalmomin
da nake maka magana. 11 Ka tafi yanzu zuwa ga 'yan'uwanka waɗanda suke zaman

§ **1:24** Da Ibraniyanci Shaddai * **1:26** Ko kuwa lafis lazuli

bauta ka yi musu magana. Ka ce musu, ‘Ga abin da Ubangiji Mai Iko Duka yana
cewa,’ ko ku ji, ko kada ku ji.”
12 Sa’an nan Ruhu ya ɗaga ni sama, a bayana na ji wata karar babban motsi na
cewa, Bari a yabi ɗaukakar Ubangiji a wurin zamansa! 13 Karar fikafikan rayayyun
halittun nan ne suke goge junansu da kuma karar da’irorin nan da suke kusa da su,
ƙarar babban motsi. 14 Sa’an nan Ruhu ya ɗaga ni sama ya kuma tafi da ni, na kuwa
tafi da ɓacin rai da kuma fushin ruhuna, tare da hannu mai ƙarfi na Ubangiji a bisa
na. 15 Na zo wurin masu zaman bautan da suke zama a Tel Abib kusa da Kogin Kebar,
A can kuwa, inda suke zama, na zauna a cikinsu kwana bakwai, ina mamaki.

### *Kashedi ga Isra’ila*
### *(Ezekiyel 33.1-9)*

16 A ƙarshen kwana bakwai ɗin maganar Ubangiji ta zo mini cewa, 17 “Ɗan mutum,
na mai da kai mai tsaro don gidan Isra’ila; saboda haka ka ji maganar da zan yi ka
kuma yi musu kashedin nan da ya fito daga gare ni. 18 In na ce wa mugu, ‘Lalle za ka
mutu,’ ba ka kuwa yi masa kashedi ko ka tsawata masa a kan mugayen hanyoyinsa
don yă ceci ransa ba, wannan mugun zai mutu saboda* zunubinsa, zan kuwa nemi
hakkin jininsa a hannunka. 19 Amma in ka yi wa mugun kashedi bai kuwa juya daga
mugayen hanyoyinsa ba, zai mutu saboda zunubinsa; amma kai kam za ka kuɓuta.
20 “Har yanzu, in mai adalci ya juya daga adalcinsa ya aikata mugunta, na kuma
sa abin tuntuɓe a gabansa, zai mutu. Da yake ba ka yi masa kashedi ba, zai mutu
saboda zunubinsa. Ba za a tuna da abin adalcin da ya yi ba, zan kuwa nemi hakkin
jininsa a hannunka. 21 Amma in ka yi wa mai adalcin kashedi kada yă yi zunubi bai
kuwa yi zunubi ba, tabbatacce zai rayu saboda ya ji kashedin, kuma kai kam za ka
kuɓuta.”
22 Hannun Ubangiji ya kasance a kaina a can, ya kuma ce mini, “Tashi ka fita zuwa
fili, a can kuwa zan yi maka magana.” 23 Saboda haka na tashi da tafi fili. Ɗaukakar
Ubangiji kuwa ta tsaya a can, kamar ɗaukakar da na gani kusa da Kogin Kebar, sai
na fāɗi rubda ciki.
24 Sai Ruhu ya sauko a kaina ya kuma ɗaga ni na tsaya a ƙafafuna. Ya yi mini
magana ya ce, “Ka fita, ka rufe kanka a cikin gida. 25 Kuma kai, ɗan mutum, za su
ɗaura ka da igiyoyi; za a ɗaure ka yadda ba za ka iya fita a cikin mutane ba. 26 Zan
sa harshenka ya manne wa dasashinka don ka yi shiru ka kuma kāsa tsawata musu,
ko da yake su gidan ’yan tawaye ne. 27 Amma sa’ad da na yi maka magana, zan buɗe
bakinka za ka kuwa faɗa musu cewa, ‘Ga abin da Ubangiji Mai Iko Duka ya faɗa.’
Duk mai ji ya ji, kuma duk wanda ya ƙi ji, ya ƙi ji; gama su gida ne na ’yan tawaye.

## 4

### *An nuna alamar kwanton ɓauna wa Urushalima*

1 “Yanzu, ɗan mutum, ka ɗauki tubalin yumɓu, ka ajiye shi a gabanka ka kuma zāna
birnin Urushalima a kansa. 2 Sa’an nan ka yi mata ƙawanya. Ka kafa mata katangar
ƙawanya, ka gina katangar da ɗan tudu ka kewaye ta da dundurusai. 3 Sa’an nan
ka ɗauki kwanon ƙarfe, ka shirya shi kamar katangar ƙarfe tsakaninka da birnin ka
kuma zuba mata ido. Za tă kasance a ƙarƙashin ƙawanya, kai kuwa za ka yi mata
ƙawanya. Wannan zai zama alama ga gidan Isra’ila.
4 “Sa’an nan ka kwanta a hagunka ka kuma sa zunubin gidan Isra’ila a kanka.*
Za ka ɗauki zunubinsu na waɗansu kwanakin da kake kwance a gefenka. 5 Na ɗora
maka kwanaki bisa ga shekarun zunubinsu. Saboda haka cikin kwana 390 za ka
ɗauki zunubin gidan Isra’ila.

---

* **3:18** Ko kuwa cikin; haka ma a ayoyi 19 da kuma 20 * **4:4** Ko kuwa a gefenka

6 “Bayan ka gama haka, ka sāke kwantawa, a wannan lokaci a gefen damarka,
ka kuma ɗauki zunubin gidan Yahuda. Na ɗora maka kwanaki 40, kwana guda a
madadin shekara guda. 7 Ka juya fuskarka wajen ƙawanyar Urushalima da hannunka
a buɗe ka yi annabci a kanta. 8 Zan ɗaura ka da igiyoyi don kada ka juya daga wannan
gefe zuwa wani gefe sai ka gama kwanakin ƙawanyarka.

9 “Ka ɗauki alkama da sha’ir, wake da acca, gero da maiwa; ka sa su a tulun ajiya
ka kuma yi amfani da su don yin burodi wa kanka. Za ka ci shi a kwanaki 390 da
za ka kwanta a gefenka. 10 Ka auna shekel ashirin na abinci don kowace rana ka
kuma ci shi a ƙayyadadden lokaci. 11 Haka ma ka auna kashi ɗaya bisa shida na
garwan ruwa ka sha shi a ƙayyadadden lokaci. 12 Ka ci abinci yadda za ka ci ƙosai
sha’ir, ka gasa shi a gaban mutane, ka yi amfani da najasar mutane kamar itacen
wuta.” 13 Ubangiji ya ce, “Ta haka mutanen Isra’ila za su ci ƙazantaccen abinci a
cikin al’ummai inda zan kore su in kai.”

14 Sai na ce, “Ba haka ba ne, Ubangiji Mai Iko Duka! Ban taɓa ƙazantar da kaina ba.
Daga ƙuruciyata har zuwa yanzu ban taɓa cin wani abin da aka samu ya mutu ko
abin da namun jeji suka kashe ba. Ba nama marar tsabtan da ya taɓa shiga bakina.”

15 Sai ya ce, “To da kyau, zan bari ka gasa burodin a kan kashin shanu a maimakon
najasar mutane.”

16 Sa’an nan ya ce mini, “Dan mutum, zan yanke tanadin abinci a Urushalima.
Mutane za su auna abincin da za su ci da tsoro su kuma auna ruwan da za su sha
cikin fargaba, 17 domin abinci da ruwa za su kāsa. Za su damu da ganin juna za su
kuma lalace saboda zunubinsu.

# 5

1 “Yanzu, ɗan mutum, ka ɗauki takobi mai kaifi ka kuma yi amfani da shi kamar
rezan mai aski don askin kanka da gemunka. Sa’an nan ka ɗauki ma’auni ka kuma
raba gashin. 2 Sa’ad da kwanakin ƙawanyarka sun ƙare, sai ka ƙone kashi ɗaya bisa
uku na gashin da wuta a cikin birnin. Ka ɗauki kashi ɗaya bisa uku ka yayyanka shi
da takobi kewaye da birnin. Ka kuma watsar da kashi ɗaya bisa uku a iska. Gama
zan fafare su da takobin da aka zāre. 3 Amma ka ɗibi gashi kaɗan ka daure a shafin
rigarka. 4 Har yanzu, ka ɗibi kaɗan na waɗannan ka zuba su cikin wuta su kuma
ƙone. Wuta zai bazu daga nan zuwa dukan gidan Isra’ila.

5 “Ga abin da Ubangiji Mai Iko Duka ya ce Urushalima ce wannan, wadda na
kafa a tsakiyar al’ummai, da ƙasashe kewaye da ita a ko’ina. 6 Duk da haka cikin
muguntarta ta yi tayarwa a kan dokokina da ƙa’idodina fiye da al’ummai da ƙasashe
kewaye da ita. Ta ƙi dokokina ba tă kuwa bi ƙa’idodina ba.

7 “Saboda haka ga abin da Ubangiji Mai Iko Duka ya ce kin yi ƙin ji fiye da al’umman
da suke kewaye da ke ba ki kuma bi ƙa’idodina ko ki kiyaye dokokina ba. Ba ki ma
dace da matsayin al’umman da suke kewaye da ke ba.

8 “Saboda haka ga abin da Ubangiji Mai Iko Duka ya ce Ni kaina ina gāba da ke,
Urushalima, kuma zan hukunta ki a gaban al’ummai. 9 Saboda dukan gumakan
banƙyamarki, zan yi abin da ban taɓa yi ba, ba kuwa zan ƙara yinsa ba. 10 Saboda
haka a cikinki ubanni za su ci ’ya’yansu, ’ya’ya kuma za su ci ubanninsu. Zan
hukunta ki zan kuma watsar da dukan waɗanda suke tsira da suke naki a iska.
11 Saboda haka muddin ina a raye, in ji Ubangiji Mai Iko Duka, domin kin ƙazantar da
wuri mai tsarkina da dukan mugayen siffofinki da kuma ayyukanki masu banƙyama,
ni kaina zan janye alherina; ba zan ji tausayinki ko in haƙura da ke ba. 12 Kashi ɗaya
bisa uku na mutanenki za su mutu da annoba ko su mutu da yunwa a cikinki; kashi
ɗaya bisa uku takobi ne zai kashe su a waje da katangarki; kashi ɗaya bisa uku kuma
zan watsar a iska in kuma fafare su da takobin da aka zāre.

13 “Sa’an nan ne fushina zai huce hasalata a kanki kuma ta lafa, in kuma wartsake.
Kuma sa’ad da na zuba fushina a kansu, a sa’an nan ne za su san cewa Ni Ubangiji
na yi magana a cikin fushin kishina a kansu.
14 “Zan mai da ki kufai da kuma abin dariya a cikin al’ummai kewaye da ke, a gaban
dukan waɗanda suke wucewa. 15 Za ki zama abin dariya da abin ba’a, kashedi da
abin banrazana ga al’ummai kewaye da ke sa’ad da na hukunta ki cikin fushi da cikin
hasala da kuma tsawatawa mai zafi. Ni Ubangiji na faɗa. 16 Sa’ad da na harbe ki da
mugayen kibiyoyina da kuma kibiyoyi masu hallakarwa na yunwa, zan yi harbi don
in kashe ki. Zan kawo ƙarin yunwa a kanki in kuma yanke tanadin abincinki. 17 Zan
aika da yunwa da namun jeji a kanki, za su kuma bar ku ba ’ya’ya. Annoba da zub
da jini za su ratsa cikinki, zan kuma kawo takobi a kanki. Ni Ubangiji na faɗa.”

## 6

*Annabci a kan duwatsun Isra’ila*

1 Maganar Ubangiji ta zo mini cewa, 2 “Dan mutum, ka kafa idonka a kan duwatsun
Isra’ila; ka yi annabci a kansu 3 ka ce, ‘Ya ku duwatsun Isra’ila, ku ji maganar
Ubangiji Mai Iko Duka. Ga abin da Ubangiji Mai Iko Duka ya ce wa duwatsu da
tuddai, ga rafuffuka da kuma kwaruruka. Ina shirin kawo takobi a kanku, kuma
zan hallaka masujadanku. 4 Za a ragargaza bagadanku a kuma farfasa bagadanku
na ƙone turare; zan kuma kashe mutanenku a gaban gumakanku. 5 Zan shimfiɗa
gawawwakin Isra’ilawa a gaban gumakansu, in kuma watsar da ƙasusuwanku
kewaye da bagadanku. 6 Duk inda kuke zama, garuruwa za su zama kango, za a
kuma ragargaza masujadai, saboda bagadanku su rurrushe su zama kango, a kuma
farfasa gumakanku su lalace, za a rurrushe bagadan ƙone turarenku, a kuma shafe
dukan abin da kuka yi. 7 Za a kashe mutanenku a cikinku, za ku kuwa sani ni ne
Ubangiji.
8 “ ‘Amma zan bar waɗansu, gama waɗansunku za su tsere wa takobi sa’ad da aka
watsar da ku a cikin ƙasashe da al’ummai. 9 Sa’an nan a cikin al’ummai inda aka kai
ku zaman bauta, waɗanda suka a tsere za su tuna da ni, yadda raina ya ɓaci ta wurin
zukatansu marasa imani, waɗanda suka rabu da ni, da kuma ta wurin idanunsu,
waɗanda suka yi sha’awace-sha’awacen gumakansu. Za su ji ƙyamar kansu saboda
mugayen abubuwan da suka aikata. 10 Za su kuwa san cewa ni ne Ubangiji; ba a
banza na ce zan kawo musu wannan masifa ba.
11 “ ‘Ga abin da Ubangiji Mai Iko Duka ya ce ku tafa hannuwanku tare ku kuma
taka ƙafafunku ku yi ihu ku ce, “Kaito!” Saboda dukan mugaye da kuma abubuwan
banƙyama na gidan Isra’ila, gama za su mutu ta wurin takobi, yunwa da annoba.
12 Wanda yake da nisa zai mutu da annoba, shi da yake kusa kuma zai mutu ta
takobi, wanda kuma ya tsira aka kuma bari zai mutu da yunwa. Ta haka zan aukar
da fushina a kansu. 13 Za su kuwa san cewa ni ne Ubangiji, sa’ad da gawawwakin
mutanensu suna kwance a kusa da gumakansu da kewaye da bagadansu, a kowane
kan tudu mai tsawo da kuma a kan dukan kan duwatsu, a ƙarƙashin kowane inuwar
itace da kuma kowane oak mai ganye, wuraren da suke ƙone turare masu ƙanshi wa
dukan gumakansu. 14 Zan kuma miƙa hannuna a kansu in mai da ƙasarsu kango daga
hamadan Dibila, a duk inda suke zama. Sa’an nan za su san cewa ni ne Ubangiji.’ ”

## 7

*Karshe ya zo*

1 Maganar Ubangiji ta zo gare ni cewa, 2 “Dan mutum, ga abin da Ubangiji Mai Iko
Duka yake cewa wa ƙasar Isra’ila,
“ ‘Karshe ya zo! Karshe ya zo

a kan kusurwoyi huɗu na ƙasar.
3 Karshe yanzu yana a kanki.
Zan fashe fushina a kanki.
Zan shari'anta ki bisa ga halinki
in sāka miki kuma saboda dukan ayyukan banƙyamar da kika yi.
4 Ba zan dube ki da tausayi;
ko in ƙyale ki ba.
Tabbatacce zan sāka miki saboda halinki
da kuma ayyukanki masu banƙyama a cikinki.
Sa'an nan za ki san cewa ni ne UBANGIJI.'

5 "Ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa,
" 'Masifa! Masifar da ba a taɓa gani ba
tana zuwa.*
6 Karshe ya zo!
Karshe ya zo!
Ya farka a kanki.
Ga shi, ya zo!
7 Kaddara ta auko miki,
ya ke wadda ke zama cikin ƙasar.
Lokaci ya yi, rana ta gabato;
akwai fargaba, ba farin ciki ba, a kan duwatsu.
8 Ina gab da fasa hasalata a kanki
in kuma aukar da fushina a kanki;
zan shari'anta ke bisa ga halinki
in kuma sāka miki saboda dukan ayyukanki masu banƙyama.
9 Ba zan dube ki da tausayi
ko in ƙyale ke ba;
zan sāka miki bisa ga halinki
da kuma ayyukan masu banƙyama a cikinki.
Sa'an nan za ki san cewa ni ne UBANGIJI wanda yake bugunki.
10 " 'Ga shi ranar ta zo!
Ta iso!
Kaddararki ta keto,
sandar ta yi toho,
girman kai ya yi fure!
11 Rikici ya yi girma ya zama
sandar da za a hukunta mugunta;
babu wani daga cikin mutanen da za a bari,
babu wani dukiyarsu da za a bari,
babu wani abin amfani.
12 Lokaci ya yi!
Ranar ta gabato!
Kada mai saya ya yi farin ciki
ko kuwa mai sayarwa ya yi baƙin ciki,
gama hasala tana a kan dukan jama'a.
13 Mai sayarwa ba zai mayar da ƙasar da ya sayar tuntuni ba
muddin dukansu suna da rai, gama ba za a sauya wahayin da ya shafi dukan jama'a ba.
Saboda zunubansu, babu ɗayansu da zai adana ransa.

* **7:5** Yawancin rubuce-rubucen hannu na Ibraniyanci da na Siriyak suna da Masifa kan masifa ne a nan

14 “ ‘Ko da yake suna busa ƙaho suna kuma shirya kome,
ba wanda zai tafi yaƙi, gama hasalata tana a kan dukan jama’a.
15 A waje takobi ne,
a ciki annoba ne da yunwa;
waɗanda suke fili za su mutu ta wurin takobi,
waɗanda kuma suke cikin birni yunwa da annoba za su cinye su.
16 Duk waɗanda suka tsira suka tsere za su kasance a cikin duwatsu,
suna kuka kamar kurciyoyin kwaruruka,
kowanne saboda zunubansa.
17 Kowane hannu zai raunana,
kowace gwiwa kuma za tă zama marar ƙarfi kamar ruwa.
18 Za su sa tufafin makoki su kuma rufu da fargaba.
Fuskokinsu kuma za su rufu da kunya a kuma aske kawunansu.

19 “ ‘Za su zubar da azurfarsu a tituna,
zinariyarsu kuma za tă zama ƙazantacciyar aba.
Azurfarsu da zinariyarsu ba za su iya cetonsu
a ranar hasalar Ubangiji ba.
Ba za su ƙosar da yunwansu ko su cika cikinsu da shi ba,
gama su ne sanadin tuntuɓensu cikin zunubi.
20 Sun yi fariya kyan kayan adonsu
suka kuma yi amfani da su don su yi gumakansu masu banƙyama,
da ƙazantattun abububuwa.
21 Zan ba da su duka kamar ganima ga baƙi
da kuma kamar abin da aka washe ga mugayen duniya,
za su kuma ƙazantar da su.
22 Zan juye fuskata daga gare su,
za su kuwa ƙazantar da wurina mai daraja;
’yan fashi za su shiga
su kuma ƙazantar da shi.

23 “ ‘Ka shirya sarƙoƙi,
domin ƙasar ta cika da alhakin jini,
birnin kuma ya cika da rikici.
24 Zan kawo al’ummai mafi mugunta su mallaki gidajenku;
zan kawo ƙarshen fariyar masu ƙarfi,
Wurare Masu Tsarkinsu za su ƙazantu.
25 Sa’ad da wahala ta zo,
za su nemi salama, amma ba za su same ta ba.
26 Masifa a kan masifa za su zo,
jita-jita kuma a kan jita-jita.
Za su yi ƙoƙarin samun wahayi daga annabi;
koyarwar doka ta wurin firist
za tă ɓace,
kamar yadda shawarar dattawa za tă ɓace.
27 Sarki zai yi makoki, yerima zai fid da zuciya,
hannuwan mutanen ƙasar kuma za su yi rawa.
Zan sāka musu bisa ga ayyukansu, zan kuma hukunta su bisa ga ma’auninsu.
Sa’an nan za su san cewa ni ne Ubangiji.’ ”

# 8

*Bautar gumaka a cikin haikali*
1 A shekara ta shida, a wata shida a ranar ta biya, yayinda nake zaune a gidana
dattawan Yahuda kuma suna zaune a gabana, hannun Ubangiji Mai Iko Duka ya zo
a kaina a can. 2 Na duba, sai na ga siffa kamar na mutum.* Daga kwankwaso zuwa
ƙasa ya yi kamar wuta, kuma daga kwankwaso zuwa sama kamanninsa ya yi haske
yana ƙyalli kamar ƙarfe mai haske. 3 Ya miƙa abin da ya yi kamar hannu ya kama a
gashin kaina. Ruhu ya ɗaga ni tsakanin sama da ƙasa, a cikin wahayoyi kuma Allah
ya ɗauke ni zuwa Urushalima, zuwa ƙofa zuwa gabas na cikin fili, inda gunki mai
tsokanar kishi yake tsaye. 4 A can gabana kuwa ga ɗaukakar Allah na Isra'ila, kamar
a wahayin da na gani a fili.
5 Sai ya ce mini, "Ɗan mutum, duba waje arewa." Sai na duba, a mashigin arewa
na ƙofar bagaden kuwa na ga wannan gunki na tsokanar kishi.
6 Ya kuma ce mini, "Ɗan mutum, ka ga abin da suke yi, abubuwan banƙyamar da
gidan Isra'ila ke yi a nan, abubuwan da za su kore ni daga wuri mai tsarkina? Amma
za ka ga abubuwan da suka ma fi banƙyama."
7 Sa'an nan ya kawo ni mashigin filin. Na duba, na kuma ga rami a bango. 8 Ya ce
mini, "Ɗan mutum, yanzu ka haƙa cikin bangon." Da na haƙa cikin bangon sai na
ga ƙofar shiga a can.
9 Sai ya ce mini, "Shiga ka ga mugaye da kuma abubuwa banƙyamar da suke yi a
can." 10 Na kuwa shiga na duba, sai na ga zāne-zāne ko'ina a bangon na kowane
irin abubuwa masu rarrafe da kuma dabbobi masu ƙazanta da dukan gumakan
gidan Isra'ila. 11 A gabansu ga dattawa saba'in na gidan Isra'ila tsaye a cikinsu,
Ya'azaniya ɗan Shafan kuwa yana tsaye a cikinsu. Kowa yana da farantin ƙona
turare a hannunsa, tulin hayaƙin turare mai ƙanshi ya tunnuƙe zuwa sama.
12 Ya ce mini, "Ɗan mutum, ka ga abin da dattawan gidan Isra'ila suke yi a cikin
duhu, kowa yana a ɗakin tsafin gunkinsa? Suna cewa, 'Ubangiji ba ya ganinmu;
Ubangiji ya yashe ƙasar.' " 13 Ya kuma ce, "Za ka gan su suna yin abubuwan da suka
fi waɗannan banƙyama."
14 Sa'an nan ya kawo ni mashigin arewa na ƙofar gidan Ubangiji, sai na ga mata
zaune a can, suna makokin Tammuz. 15 Ya ce mini, "Ɗan mutum, ka ga wannan? Za
ka ga abubuwan da suke masu banƙyama fiye da wannan."
16 Sa'an nan ya kawo ni cikin fili na cikin gidan Ubangiji, a can kuwa a ƙofar haikali,
tsakanin shirayi da bagade, akwai kamar mutum ashirin da biyar. Suka ba haikalin
Ubangiji baya suna fuskanta wajen gabas, suna rusuna wa rana a gabas.
17 Ya ce mini, "Ka ga wannan, ɗan mutum? Karamin abu ne gidan Yahuda su yi
abubuwan banƙyamar da suke yi a nan? Dole ne su cika ƙasar da rikici su kuma ci
gaba da tsokane ni in yi fushi? Dube su suna tsokanata! 18 Saboda haka zan hukunta
su cikin fushi; Ba zan dube su da tausayi ko kuwa in ƙyale su ba. Ko da yake suna
ihu a kunnuwana, ba zan saurare su ba."

# 9

*An kashe masu bautar gumaka*
1 Sai na ji ya yi kira da babbar murya yana cewa, "Kawo matsaran birni a nan,
kowanne da makami a hannunsa." 2 Na kuma ga mutane shida suna zuwa daga
kowane gefen ƙofar ta bisa, wadda take fuskantar arewa, kowanne da makamin kisa
a hannunsa. Tare da su akwai mutum saye da lilin yana rataye da jaka ƙunshe da
kayan rubutu a gefensa. Suka shiga suka tsaya kusa da bagaden tagulla.

* **8:2** Ko kuwa na ga siffa mai kamanni wuta

3 To, fa, ɗaukakar Allah na Isra’ila ta haura daga bisa kerubobi, inda ta kasance,
ta tashi zuwa bakin madogarar ƙofar haikali. Sai Ubangiji ya kira mutumin da yake
saye da lilin wanda ya rataye jaka ƙunshe da kayan rubutu a gefensa 4 ya ce masa,
“Ka ratsa birnin Urushalima ka sa shaida a goshin waɗanda suke baƙin ciki da kuma
makoki a kan dukan abubuwan banƙyamar da ake yi a cikinsa.”
5 Yayinda nake saurara, sai ya ce wa waɗansu, “Ku bi shi ta birnin ku kuma kashe,
babu tausayi ko kuwa jinƙai. 6 Ku kashe tsofaffi da samari da ’yan mata, mata da
yara, amma kada ku taɓa wani wanda yake da shaida. Ku fara a wuri mai tsarkina.”
Saboda haka suka fara da dattawan da suke gaban haikali.
7 Sa’an nan ya ce musu, “Ku ƙazantar da haikalin ku kuma cika filayen da kisassu.
Ku tafi!” Saboda haka suka fita suka kuma fara kisa a duk birnin. 8 Yayinda suke kisan
sai aka bar ni kaɗai, na fāɗi rubda ciki, na yi kuka na ce, “Kash, Ubangiji Mai Iko
Duka! Za ka hallaka dukan raguwar Isra’ila a wannan zafin fushinka a Urushalima?”
9 Ya amsa mini ya ce, “Zunubin gidan Isra’ila da Yahuda ya yi girma ainun; ƙasar
ta cika da rashin adalci. Suna cewa, ‘Ubangiji ya yashe ƙasar; Ubangiji ba ya gani.’
10 Saboda haka ba zan dube su da tausayi ko kuwa in ƙyale su ba, amma zan kawo
wa kansu abin da suka yi.”
11 Sai mutumin da yana saye da lilin yake kuma rataye da jaka ƙunshe da kayan
rubutu a gefensa ya mayar da magana, yana cewa, “Na yi yadda ka umarci ni.”

# 10

*Daukaka ta rabu da haikali*

1 Na duba, sai na ga kamannin kursiyin saffaya* a kan sararin da yake a bisa
kawunan kerubobi. 2 Sai Ubangiji ya ce wa mutumin da yake saye da lilin, “Ka shiga
cikin da’irorin da suke ƙarƙashin kerubobi. Ka cika hannuwanka da garwashin wuta
wanda yake tsakanin kerubobin ka kuma watsar da su a kan birnin.” Yayinda nake
dubawa, sai ya shiga.
3 Kerubobin kuwa suna tsaye a gefen kudu na haikali sa’ad da mutumin ya shiga,
sai girgije ya cika filin da yake can ciki. 4 Sai ɗaukakar Ubangiji ya tashi daga bisa
kerubobi ya tafi zuwa madogarar ƙofar haikali. Girgijen ya cika haikali, filin kuwa
ya cika da hasken ɗaukakar Ubangiji. 5 Sai aka ji ƙarar fikafikan kerubobin har a
filin waje, kamar muryar Allah Maɗaukaki† sa’ad da ya yi magana.
6 Sa’ad da Ubangiji ya umarci mutumin da yake saye da lilin cewa, “Ka ɗibi wuta
daga cikin tsakanin da’irorin, daga tsakanin kerubobin,” sai mutumin ya shiga ya
tsaya kusa da da’irar. 7 Sa’an nan ɗaya daga cikin kerubobin ya miƙa hannu zuwa
wurin wutar da take tsakaninsu. Ya ɗebo wutar daga ciki ya zuba a hannuwan
mutumin da yake saye da lilin, shi kuwa ya karɓa ya fita. 8 (A ƙarƙashin fikafikan
kerubobin ana iya ganin abin da ya yi kamar hannuwan mutum.)
9 Na duba, sai na ga kusa da kerubobin akwai da’irori huɗu, kowanne kusa da kerub
guda; da’irorin suna ƙyalli kamar wani dutse mai daraja. 10 Game da kamanninsu
kuwa, huɗu a cikinsu sun yi kama da juna; kowanne ya yi kamar da da’ira a cikin
da’ira. 11 Yayinda suke tafiya, sukan tafi kowane gefe huɗun da kerubobin suka nufa;
da’irorin ba sa juyawa yayinda kerubobin suke tafiya. Kerubobin suka tafi kowane
gefen da kan ya nufa, ba tare da juyawa ba sa’ad da suke tafiya. 12 Jikunansu gaba
ɗaya, har da bayansu, hannuwansu da fikafikansu, sun cika gaba ɗaya da idanu,
kamar yadda suke a da’irori huɗun. 13 Na ji ana kiran da’irorin “da’irorin guguwa.”
14 Kowane daga kerubobin yana da fuskoki huɗu. Fuska ɗaya na kerub ne, na biyun
fuskar mutum ne, na ukun fuskar zaki ne, na huɗun kuwa fuskar gaggafa ce.

* **10:1** Ko kuwa lafis lazuli † **10:5** Da Ibraniyanci El-Shaddai

[15] Sai kerubobin suka tashi sama. Waɗannan ne halittu masu ran da na gani kusa
da Kogin Kebar. [16] Sa'ad da kerubobin suka motsa, sai da'irorin da suke kusa da su
su motsa; kuma sa'ad da kerubobin suka buɗe fikafikansu don su tashi daga ƙasa,
da'irorin ba sa barin wurarensu. [17] Sa'ad da kerubobin suka tsaya cik, su ma sukan
tsaya cik; kuma sa'ad da kerubobin suka tashi, sai su ma su tashi tare da su, domin
ruhun rayayyun halittun yana a cikinsu.
[18] Sai ɗaukakar UBANGIJI ya tashi daga bisa madogarar ƙofar haikali ya kuma tsaya
a bisa kerubobi. [19] Yayinda nake duba, kerubobin suka buɗe fikafikansu suka kuma
tashi daga ƙasa, yayinda suka tafi kuwa, da'irorin suka tafi tare da su. Suka tsaya
a mashigin ƙofar gabas na gidan UBANGIJI, ɗaukakar Allah na Isra'ila kuwa yana a
kansu.
[20] Waɗannan ne rayayyun halittun da na gani a ƙarƙashin Allah na Isra'ila kusa da
Kogin Kebar, na kuma gane cewa su kerubobi ne. [21] Kowanne yana da fuskoki huɗu
da fikafikai huɗu, a ƙarƙashin kuwa akwai wani abin da ya yi kamar hannuwan
mutum. [22] Fuskokinsu suna da kamanni ɗaya da waɗanda na gani kusa da Kogin
Kebar. Kowanne ya tafi kai tsaye sosai.

# 11

### *Hukuncin shugabannin Isra'ila*

[1] Sa'an nan Ruhu ya ɗaga ni sama ya kawo ni ƙofar gidan UBANGIJI wadda take
fuskantar gabas. Can a mashigi zuwa ƙofar akwai mutum ashirin da biyar, na kuma
ga a cikinsu akwai Ya'azaniya ɗan Azzur da Felatiya ɗan Benahiya, shugabannin
jama'a. [2] UBANGIJI ya ce mini, "Ɗan mutum, waɗannan su ne mutanen da suke ƙulla
mugunta suna kuma ba da muguwa shawara a cikin wannan birni. [3] Suna cewa,
'Lokaci bai yi kusa da za a gina gidaje ba?* Wannan birni yana tukunyar dahuwa,
mu ne kuwa naman.' [4] Saboda haka yi annabci a kansu; yi annabci, ɗan mutum."
[5] Sai Ruhun UBANGIJI ya sauko a kaina, ya kuma faɗa mini in ce, "Ga abin da
UBANGIJI yana cewa, haka kuke cewa, ya gidan Isra'ila, amma na san abin da yake a
zuciyarku. [6] Kun kashe mutane da yawa a wannan birni kuka kuma cika titunanta
da gawawwaki.
[7] "Saboda haka ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa gawawwakin da kuka
zubar a can su ne naman, wannan birni kuwa ita ce tukunya, amma zan kore ku daga
cikinta. [8] Kuna jin tsoron takobi, kuma takobi ne zan kawo muku, in ji UBANGIJI Mai
Iko Duka. [9] Zan kore ku daga birnin in miƙa ku a hannuwan baƙi in kuma azabtar
da ku. [10] Za ku mutu ta wurin takobi, zan kuma hukunta ku a iyakokin Isra'ila. Sa'an
nan za ku san cewa ni ne UBANGIJI. [11] Wannan birni ba za tă zama muku tukunya ba,
ba kuwa za ku zama nama a cikinta ba; zan hukunta ku a iyakokin Isra'ila. [12] Za ku
kuwa san cewa ni ne UBANGIJI, gama ba ku bi ƙa'idodina ba balle ku kiyaye dokokina,
amma kuka bi hanyoyin al'ummai kewaye da ku."
[13] Yanzu yayinda nake yin annabci, sai Felatiya ɗan Benahiya ya mutu. Sai na fāɗi
rubda ciki na kuma yi kuka da babbar murya na ce, "Kash, UBANGIJI Mai Iko Duka!
Za ka hallaka raguwar Isra'ila ƙaƙaf ne?"
[14] Sai maganar UBANGIJI ta zo mini cewa, [15] "Ɗan mutum, 'yan'uwanka,
'yan'uwanka waɗanda suke danginka na cikinka† da kuma dukan gidan Isra'ila su
ne waɗanda mutanen Urushalima suka ce, 'Su ne‡ da nisa daga UBANGIJI; an ba mu
wannan ƙasa ta zama mallakarmu.'

### *Alkawarin komowar Isra'ila*

* **11:3** Ko kuwa Wannan ba lokacin gina gidaje ba ne † **11:15** Ko kuwa suke zaman bauta tare da kai (dubi Seftuwajin da kuma Siriyak) ‡ **11:15** Ko kuwa waɗanda mutanen Urushalima suka ce, "Tsaya"

[16] “Saboda haka ka ce, ‘Ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa ko da yake
na kore su zuwa cikin al’ummai na kuma warwatsa su cikin ƙasashe, duk da haka
na zama wuri mai tsarki a gare su a ƙasashen da suka tafi.’
[17] “Saboda haka, ka ce, ‘Ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa zan tattaro ku
daga al’ummai in kuma dawo da ku daga ƙasashen da aka warwatsa ku, zan kuwa
sāke mayar muku da ƙasar Isra’ila.’
[18] “Za su dawo gare ta su kawar da dukan mugayen siffofi da gumaka masu
banƙyama. [19] Zan ba su zuciya ɗaya in kuma sa sabon ruhu a cikinsu; zan fid
da zuciyar dutse daga gare su in kuma ba su zuciya ta nama. [20] Sa’an nan za su
bi ƙa’idodina su kuma yi hankali ga kiyaye dokokina. Za su zama mutanena, ni
kuwa zan zama Allahnsu. [21] Amma game da waɗanda zukatansu suka karkata ga bin
mugayen siffofi da gumakan banƙyama, zan sāka musu gwargwadon ayyukansu, in
ji UBANGIJI Mai Iko Duka.”
[22] Sa’an nan kerubobi, tare da da’irori kusa da su, suka buɗe fikafikansu, ɗaukakar
Allah kuwa tana a bisansu. [23] Ɗaukakar UBANGIJI ta haura daga cikin birnin ta sauka
a bisa dutse gabas da shi. [24] Ruhu ya ɗaga ni sama ya kuma kawo ni ga masu zaman
bauta a ƙasar Babilon§ cikin wahayin da Ruhun Allah ya bayar.
Sa’an nan wahayin da na gani ya rabu da ni, [25] na kuwa faɗa wa masu zaman
bautan dukan abin da UBANGIJI ya nuna mini.

# 12

*An yi alamar zaman bauta*

[1] Maganar UBANGIJI ta zo mini cewa [2] ɗan mutum, kana zama a cikin mutane masu
tawaye, Suna da idanun gani amma ba sa gani, suna da kunnuwan ji amma ba sa ji,
gama ’yan tawaye ne.
[3] “Saboda haka ɗan mutum, ka tattara kayanka don zuwa zaman bauta, ka tashi
da rana suna gani ka ƙaura a inda kake zuwa wani wuri. Mai yiwuwa za su gane,
ko da yake su gidan ’yan tawaye ne. [4] Da rana, yayinda suke kallo, ka fid da kayanka
da ka tattara don zuwa zaman bauta. Sa’an nan da yamma, yayinda suke kallo, ka
fita kamar yadda mutane masu tafiyar zaman bauta sukan yi. [5] Yayinda suke kallo,
ka huda katanga ka fitar da kayanka daga ciki. [6] Ka sa su a kafaɗarka yayinda suke
kallo ka kuma fitar da su da dare. Ka rufe fuskarka don kada ka ga ƙasar, gama na
mai da kai alama ga gidan Isra’ila.”
[7] Sai na yi kamar yadda aka umarce ni. Da rana na fitar da kayana da na tattara
don zuwa zaman bauta. Sa’an nan da yamma na huda katanga da hannuwana. Na
kwashe kayana da dare, na ɗauke su a kafaɗuna yayinda suke kallo.
[8] Da safe maganar UBANGIJI ta zo mini cewa, [9] “Ɗan mutum, gidan ’yan tawayen
nan na Isra’ila ba su tambaye ka, ‘Me kake yi ba?’
[10] “Ka ce musu, ‘Ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa wannan abin da
Allah ya yi magana a kai ya shafi sarki a Urushalima da kuma dukan gidan Isra’ila
waɗanda suke a can.’ [11] Ka ce musu, ‘Ni alama ne a gare ku.’
“Kamar yadda na yi, haka za a yi da su. Za a kai su zaman bauta kamar kamammu.
[12] “Sarkin da yake a cikinsu zai ɗauki kayansa ya saɓa a kafaɗarsa da dare ya tafi,
za a huda masa rami a katanga ya fita. Zai rufe fuskarsa don kada yǎ ga ƙasar. [13] Zan
shimfiɗa masa ragata, za a kuwa kama shi da tarkona; zan kawo shi Babiloniya,
ƙasar Kaldiyawa, amma ba zai gan ta ba, a can kuwa zai mutu. [14] Zan warwatsa
dukan waɗanda suke kewaye da shi a dukan fuskokin iska, ma’aikatansa da dukan
rundunoninsa, zan fafare su da takobin da aka zāre.

§ **11:24** Ko kuwa Kaldiyawa

15 “Za su san cewa ni ne UBANGIJI sa’ad da na watsar da su a cikin al’ummai na
kuma warwatsa su cikin ƙasashe. 16 Amma zan bar kaɗan daga cikinsu su tsere
wa takobi, yunwa da annoba, saboda a cikin al’umman da suka tafi su furta dukan
ayyukansu masu banƙyama. Sa’an nan za su san cewa ni ne UBANGIJI.”
17 Maganar UBANGIJI ta zo mini cewa, 18 “Ɗan mutum, ka yi rawar jiki yayinda kake
cin abincinka, ka kuma yi makyarkyata don tsoro yayinda kake shan ruwanka. 19 Ka
faɗa wa mutanen ƙasar cewa, ‘Ga abin UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa game da
waɗanda suke zama a Urushalima da kuma cikin ƙasar Isra’ila. Za su ci abincinsu
da razana, su sha ruwansu da tsoro, gama za a washe dukan abin da yake ƙasarsu
saboda hargitsin dukan waɗanda suna zama a can. 20 Garuruwan da mutane suna
ciki za su zama kufai ƙasar kuma za tă zama kango. Sa’an nan za ku san cewa ni ne
UBANGIJI.’ ”
21 Maganar UBANGIJI ta zo mini cewa, 22 “Ɗan mutum, mene ne wannan karin
magana da kuke da shi a ƙasar Isra’ila mai cewa, ‘Kwanaki suna ta wucewa, wahayi
bai gudana ba’? 23 Ka ce musu, ‘Ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa zan
kawo ƙarshen wannan karin magana, ba za su ƙara faɗar wannan karin magana a
Isra’ila ba.’ Ka ce musu, ‘Kwanaki sun gabato da za a tabbatar da kowane wahayi.
24 Gama ba za a ƙara ganin wahayin ƙarya ko a yi duba na daɗin baki a cikin mutanen
Isra’ila ba. 25 Amma Ni UBANGIJI zan yi magana abin da na nufa, za tă kuwa tabbata
ba tare da jinkiri ba. Gama cikin kwanakinku, kai gidan ’yan tawaye, zan cika duk
abin da na faɗa, in ji UBANGIJI Mai Iko Duka.’ ”
26 Maganar UBANGIJI ta zo mini cewa, 27 “Ɗan mutum, gidan Isra’ila suna cewa,
‘Wahayin da yake gani na shekaru masu yawa ne nan gaba, yana kuma annabce-
annabce game da wani zamani ne can.’
28 “Saboda haka ka ce musu, ‘Ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yake cewa ba wata
maganata da za tă ƙara yin jinkiri; duk abin da na faɗa zai cika, in ji UBANGIJI Mai
Iko Duka.’ ”

# 13

*An hukunta annabawan ƙarya*

1 Maganar UBANGIJI ta zo mini cewa, 2 “Ɗan mutum, yi annabci a kan annabawan
Isra’ila waɗanda suke annabci yanzu. Ka faɗa wa waɗanda suke annabci bisa ga
ra’ayinsu cewa, ‘Ku ji maganar UBANGIJI! 3 Ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yake
faɗa, Kaiton wawaye annabawan da suke bin ruhunsu kuma ba su ga kome ba!
4 Annabawanki, ya Isra’ila, suna kama da diloli a kufai. 5 Ba ku haura don ku rushe
katanga don ku gyara gidan Isra’ila saboda ya tsaya daram a yaƙi a ranar UBANGIJI
ba. 6 Wahayoyinsu ƙarya ne suna yin dubansu na ƙarya ne. Sukan ce, UBANGIJI ya
furta, alhali kuwa UBANGIJI bai aike su ba; duk da haka sukan sa zuciya ga cikawar
maganarsu. 7 Ba ku ga wahayin ƙarya kuka kuma faɗa yin duban ƙarya sa’ad da
kuka ce, “UBANGIJI ya furta,” ko da yake bai yi magana ba?
8 “ ‘Saboda haka ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa saboda maganga-
nunku na ƙarya da wahayinku na ƙarya, ina gāba da ku, in ji UBANGIJI Mai Iko Duka.
9 Hannuna zai yi gāba da annabawan da suke ganin wahayin ƙarya suna kuma yin
duban ƙarya. Ba za su kasance cikin taron mutanena ba, ba kuwa za a rubuta su a
littafin gidan Isra’ila ba, ba za su shiga ƙasar Isra’ila ba. Ta haka za ku san cewa ni
ne UBANGIJI Mai Iko Duka.
10 “ ‘Domin sun ɓad da mutanena, suna cewa, “Salama,” sa’ad da ba salama, kuma
saboda, sa’ad da ana gina katanga marar ƙarfi, sukan shafe ta da farar ƙasa, 11 saboda
haka ka faɗa wa waɗanda suka shafe da farar ƙasa cewa za tă fāɗi. Ruwan sama zai
sauko da rigyawa, zan kuma aika da ƙanƙara, kuma babbar iska za tă ɓarke. 12 Sa’ad

da katangar ta fāɗi, mutane ba za su tambaye ku ba cewa, “Ina shafen farar ƙasar
da kuka yi mata?”
13 “ ‘Saboda haka ga abin da Ubangiji Mai Iko Duka yana cewa a cikin hasalata
zan saki babbar iska, kuma cikin fushina zan tura ƙanƙara kuma rigyawan ruwan
sama zai sauko da fushin hallaka. 14 Zan rushe katangar da kuka shafe da farar ƙasa
zan baje ta har ƙasa saboda tushenta zai tsaya tsirara. Sa’ad da ta fāɗi, za a hallaka
ku a cikinta; kuma za ku san cewa ni ne Ubangiji Mai Iko Duka. 15 Ta haka zan
aukar wa katangar da hasalata da kuma a kan waɗanda suka yi shafenta da farar
ƙasa. Zan ce muku, “Katangar ta fāɗi haka kuma mutanen da suka shafe ta da farar
ƙasa, 16 waɗannan annabawan Isra’ila waɗanda suka yi annabci wa Urushalima suka
kuma ga mata wahayin salama sa’ad da ba salama, in ji Ubangiji Mai Iko Duka.” ’
17 “To, ɗan mutum, ka kafa idonka a kan ’yan matan mutanenka waɗanda suke
annabci bisa ga ra’ayinsu. Yi annabci a kansu 18 ka kuma ce, ‘Ga abin da Ubangiji Mai
Iko Duka yana cewa kaiton matan da suke ɗinka kambuna a hannuwansu suna kuma
yin gyale masu tsawo dabam-dabam wa kawunansu don su farauci mutane. Za ku
farauci rayukan mutanena ku bar naku? 19 Kun jawo mini kunya a cikin mutanena
don a tafa muku sha’ir da ɗan dunƙulen burodi. Ta wurin yin ƙarya wa mutanena,
waɗanda suke jin ƙarairayi, kuka kashe waɗanda bai kamata su mutu ba kuka bar
waɗanda ya kamata su mutu.
20 “ ‘Saboda haka ga abin da Ubangiji Mai Iko Duka yana cewa ina gāba da
kambunanku waɗanda kuke farautar mutane da su kamar tsuntsaye don haka zan
kuma tsintsinke su daga hannuwanku; zan ’yantar da mutanen da kuka farauto
kamar tsuntsaye. 21 Zan kyakketa gyalenku in ceci mutanena daga hannuwanku,
ba za su kuma ƙara zama ganima a hannunku ba. Sa’an nan za ku san cewa ni ne
Ubangiji 22 Domin kun karya zuciyar masu adalci da ƙarairayinku, sa’ad da na fitar
da su babu damuwa, kuma domin kun ƙarfafa mugaye kada su juye daga mugayen
hanyoyinsu su ceci rayukansu, 23 saboda haka ba za ku ƙara ganin wahayin ƙarya
ba, ko ku yi duba. Zan ceci mutanena daga hannuwanku. A sa’an nan za ku san
cewa ni ne Ubangiji.’ ”

# 14

*An ƙi masu bautar gumaka*

1 Waɗansu dattawan Isra’ila suka zo wurina suka zauna a ƙasa a gabana. 2 Sai
maganar Ubangiji ta zo mini cewa, 3 “Ɗan mutum, waɗannan mutane sun kafa
gumaka a cikin zukatansu suka sa mugayen abubuwan sa tuntuɓe a gabansu. Zan
bar su, su taɓa nemi ni? 4 Saboda haka ka yi musu magana ka faɗa musu cewa,
‘Ga abin da Ubangiji Mai Iko Duka yana cewa sa’ad da wani mutumin Isra’ila ya
kafa gumaka a cikin zuciyarsa ya kuma sa mugun abin tuntuɓe a gabansa sa’an nan
ya tafi wurin annabi, Ni Ubangiji zan amsa masa da kaina game da babban bautar
gumakarsa. 5 Zan yi haka don in sāke ƙame zukatan mutanen Isra’ila, waɗanda duk
suka yashe ni don gumakansu.’
6 “Saboda haka ka faɗa wa gidan Isra’ila cewa, ‘Ga abin da Ubangiji Mai Iko Duka
yana cewa ku tuba! Ku juyo daga gumakanku ku kuma furta dukan ayyukanku masu
banƙyama!
7 “ ‘Duk sa’ad da mutumin Isra’ila ko baƙo mai zama a Isra’ila ya rabu da ni ya
kuma kafa gumaka a cikin zuciyarsa ya kuna sa mugun abin tuntuɓe a gabansa
sa’an nan ya tafi wurin annabi don yă neme ni, Ni Ubangiji zan amsa masa da kaina.
8 Zan yi gāba da mutumin in kuma sa ya zama misali da kuma abin karin magana.
Zan ware shi daga mutanena. Sa’an nan za ku san cewa ni ne Ubangiji.

[9] " 'In kuma aka ruɗi annabin har ya yi annabci, Ni UBANGIJI na rinjayi wannan
annabi, zan kuma miƙa hannuna gāba da shi in hallaka shi daga cikin mutanena
Isra'ila. [10] Za su ɗauki hakkin laifinsu annabin zai zama mai laifi daidai da wanda ya
zo neman shawararsa. [11] Sa'an nan mutanen Isra'ila ba za su ƙara kauce daga gare
ni ba, ba kuwa za su ƙara ƙazantar da kansu da dukan zunubansu ba. Za su zama
mutanena, ni kuma zan zama Allahnsu, in ji UBANGIJI Mai Iko Duka.' "

*Hukuncin Urushalima babu makawa*

[12] Maganar UBANGIJI ta zo mini cewa, [13] "Ɗan mutum, in wata ƙasa ta yi mini
zunubi ta wurin rashin aminci na kuma miƙa hannuna gāba da ita don in toshe
hanyar samun abincinta na kuma aika da yunwa a kanta na kashe mutanenta da
dabbobinta, [14] ko da waɗannan mutum uku Nuhu, Daniyel* da kuma Ayuba suna a
cikinta, za su iya ceton kansu ne kawai ta wurin adalcinsu, in ji UBANGIJI Mai Iko
Duka.

[15] "Ko kuwa in na aika da namun jeji su ratsa cikin wannan ƙasa suka kuma bar
ta babu yaro, ta kuma zama kufai har babu wanda zai ratsa cikinta saboda namun
jeji, [16] muddin ina raye, in ji UBANGIJI Mai Iko Duka, ko da ma waɗannan mutum uku
suna a cikinta, ba za su iya ceton 'ya'yansu maza ko mata ba. Su kaɗai za a iya ceto,
amma ƙasar za tă zama kufai.

[17] "Ko kuma in na kawo takobi a kan wannan ƙasa na kuma ce, 'Bari takobin ya
ratsa cikin dukan ƙasar,' na kuma kashe mutanenta da dabbobinsu, [18] muddin ina
raye, in ji UBANGIJI Mai Iko Duka, ko da waɗannan mutum uku suna cikinta, ba za su
iya ceton 'ya'yansu maza ko mata ba. Su kaɗai za a iya ceto.

[19] "Ko kuma in na aika da annoba a cikin wannan ƙasa na kuma yi fushi a kanta
ta wurin kisa, ina kisan mutanenta da dabbobinsu, [20] muddin ina raye, in ji UBANGIJI
Mai Iko Duka, ko da Nuhu, Daniyel da Ayuba suna a cikinta, ba za su iya ceton ɗansu
ko 'yarsu ba. Za su iya ceton kansu ne kaɗai ta wurin adalcinsu.

[21] "Gama ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa balle fa sa'ad da na aika wa
Urushalima da hukuntaina guda huɗu masu zafi takobi da yunwa da namun jeji da
annoba don su kashe mutanenta da dabbobinsu! [22] Duk da haka za a sami mutanen
da za su ragu 'ya'ya maza da matan da za a fitar daga cikinta. Za su zo wurinka,
kuma sa'ad da ka gan halinsu da ayyukansu, za ka ta'azantu game da bala'in da na
kawo a kan Urushalima kowane bala'in da na kawo a kanta. [23] Za ka ta'azantu sa'ad
da ka ga halinsu da kuma ayyukansu, gama za ka san cewa ban aikata wani abu a
cikinta ba dalili ba, in ji UBANGIJI Mai Iko Duka."

# 15

*Urushalima, kuringa marar amfani*

[1] Maganar UBANGIJI ta zo mini cewa, [2] "Ɗan mutum, da me itacen kuringa ya fi
reshen waɗansu itatuwa kyau a cikin kurmi? [3] An taɓa ɗaukan itacensa an yi wani
abu mai amfani? Akan yi maratayi da ita da za a rataya wani abu a kai? [4] Bayan kuma
a jefa ta cikin wuta, wuta kuma ta cinye kowane gefe ta kuma babbaka tsakiyarta,
tana da amfani don yin wani abu kuma? [5] In ba ta da amfanin wani abu sa'ad da
take cikakkiya, balle bayan da wuta ta babbake ta, za a iya yin amfani da ita?

[6] "Saboda haka ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa kamar yadda na ba da
itacen kuringa a cikin itatuwan kurmi ya zama itacen wuta, haka zan sa mazaunan
Urushalima su zama. [7] Zan yi gāba da su. Ko da yake sun fito daga wuta, wuta za tă
cinye su. Kuma sa'ad da na yi gāba da su, za ku san cewa ni ne UBANGIJI. [8] Zan mai
da ƙasar kufai domin sun yi rashin aminci, in ji UBANGIJI Mai Iko Duka."

* **14:14** Ko kuwa Danel; yadda aka rubuta sunan da Ibraniyanci mai yiwuwa yana nuna wani ne dabam da annabi Daniyel, haka ma a aya 20

# 16

### *Misalin rashin amincin Urushalima*

1 Maganar UBANGIJI ta zo mini cewa, 2 “Ɗan mutum, ka sa Urushalima ta san
ayyukanta masu banƙyama 3 ka ce, ‘Ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa wa
Urushalima, Asalinki da haihuwarki daga ƙasar Kan’ana ne; mahaifinki mutumin
Amoriyawa ne, mahaifiyarki kuma mutuniyar Hitti ce. 4 A ranar da aka haife ki ba a
yanke cibiyarki ba, ba a kuma yi miki wanka don a tsabtacce ki ba, ba a kuma goge
ki da gishiri ba ko a naɗe ki cikin tsummoki. 5 Ba wanda ya dube ki da tausayi ko
ya nuna miki isashen jinƙai don yǎ yi miki ɗaya daga cikin waɗannan abubuwa. A
maimako, sai aka jefar da ke a fili, gama a ranar da aka haife ki an ji ƙyamarki.
6 “ ‘Sa’an nan na wuce na ga kina birgima cikin jininki, yayinda kike kwance can
cikin jininki sai na ce miki, “Ki rayu!”[*] 7 Na sa kin yi girma kamar tsiro a fili. Kin yi
girma kika kuma yi tsayi kika zama mafiya kyau na kayan ado.[†] Nononki suka fito,
gashinki kuwa suka yi girma, duk da haka tsirara kike tik.
8 “ ‘Daga baya na wuce, da na dube ki sai na ga cewa kin yi girma sosai har kin kai
a ƙaunace ki, na yafa gefen tufafina a kanki na kuma rufe tsiraincinki. Na rantse
miki, na ƙulla alkawari da ke, kin kuwa zama tawa, in ji UBANGIJI Mai Iko Duka.
9 “ ‘Na yi miki wanka na wanke miki jini daga gare ki na kuma shafa miki mai.
10 Na rufe ki da rigar da aka yi wa ado na kuma sa miki takalman fata. Na sa miki
riga ta lilin mai kyau na kuma rufe ki da riguna masu tsada. 11 Na yi miki ado da
kayan ado masu daraja, na sa miki mundaye a hannuwanki da abin wuya a wuyanki,
12 na kuma sa miki zobe a hancinki, abin kunne a kunnuwanki da rawani mai kyau
a kanki. 13 Haka kuwa aka caɓa miki zinariya da azurfa; tufafinki kuwa na lilin mai
kyau da riguna masu tsada waɗanda aka yi musu ado. Abincinki na gari mai laushi
ne, zuma da man zaitun. Kika zama kyakkyawa har kika kuma zama sarauniya.
14 Sunanki ya yaɗu a cikin al’ummai saboda kyanki, domin darajar da na ba ki ya sa
kyanki ya zama cikakke, in ji UBANGIJI Mai Iko Duka.
15 “ ‘Amma kika dogara ga kyanki kika kuma yi amfani da sunan da kika yi don ki
zama karuwa. Kin yi ta jibga alherai a kan kowa da ya wuce, sai kyanki ya zama naki.
16 Kin ɗauki waɗansu tufafinki don ki yi wa kanki masujadai masu ado, inda kike
karuwancinki. Irin waɗannan abubuwa bai kamata su faru ba, bai kuma kamata su
taɓa faruwa ba. 17 Kika kuma ɗauki kayan ado masu kyau da na ba ki, kayan adon
da aka yi da zinariya da azurfa, kika yi wa kanki gumakan maza kika kuma yi ta yin
karuwanci da su. 18 Kika ɗauki rigunanki masu ado don ki sa a kansu, kika kuma
miƙa maina da turarena a gabansu. 19 Haka ma abincin da na tanada miki, lallausan
gari, man zaitun, da zuman da na ba ki ki ci, kin miƙa su kamar turare mai ƙanshi
a gabansu, in ji UBANGIJI Mai Iko Duka.
20 “ ‘Kika kuma kwashe ’ya’yanki maza da mata waɗanda kin haifa mini kika
miƙa su kamar abinci ga gumakanki. Karuwancinki bai isa ba ne? 21 Kin kashe
’ya’yana kika kuma miƙa su[‡] ga gumaka. 22 Cikin dukan ayyukan banƙyamarki da
karuwancinki ba ki tuna da kwanakin ƙuruciyarki ba, sa’ad da kike tsirara tik, kina
birgima cikin jininki.
23 “ ‘Kaito! Kaitonki, in ji UBANGIJI Mai Iko Duka. Bugu da ƙari a kan dukan
waɗansu muguntarki, 24 kin gina wa kanki ɗakunan sama da gidajen tsafi a kowane
dandali. 25 A kowane titi kin gina ɗakin tsafi kika kuma wulaƙanta kyanki, kina miƙa
jikinki da ƙarin fasikanci ga duk mai wucewa. 26 Kin yi karuwanci da Masarawa,

---

[*] **16:6** Kaɗan cikin rubuce-rubucen Ibraniyanci, Seftuwajin, da kuma Siriyak; yawancin rubuce-rubucen Ibraniyanci na da “Ki rayu!” Kuma yayinda kike kwance cikin jininki na ce miki, “Ki rayu!” [†] **16:7** Ko kuwa kika zama budurwa [‡] **16:21** Ko kuwa kika kuma sa suka wuce ta cikin wuta

maƙwabtanki masu kwaɗayi, kika tsokane ni har na yi fushi da ƙarin fasikancinki.
27 Saboda haka na miƙa hannuna gāba da ke na kuma rage iyakarki; na ba da ke ga
abokan gābanki masu haɗama, 'yan matan Filistiyawa, waɗanda suka sha mamaki
saboda halinki na lalata. 28 Kin kuma yi karuwanci da Assuriyawa, domin ba kya
ƙoshi; kai ko bayan wannan, ba ki ƙoshi ba. 29 Sai kika ƙara fasikancinki da ya haɗa
da ƙasar cinikin Babilon,§ amma duk da haka ba ki ƙoshi ba.
30 " 'Kina da rashin ƙarfi a zuci, in ji UBANGIJI Mai Iko Duka, sa'ad da kika yi duk
waɗannan abubuwa, kina yi kamar karuwar da aka watsa! 31 Sa'ad da kika gina
ɗakunan samanki a kowane gefen titi kika kuma gina ɗakunan tsafinki a kowane
dandali, ba kamar karuwa kike ba, domin kin karɓi kuɗi.
32 " 'Ke mazinaciyar mace! Kin gwammace baƙi a maimakon mijinki! 33 Kowace
karuwa kan karɓi kuɗi, amma kina ba da kyautai ga dukan kwartayenki, kina ba
su cin hanci don su zo wurinki daga ko'ina don alherai marasa ƙa'ida. 34 Saboda
haka cikin karuwancinki kin sha bamban da saura; babu wanda yake binki saboda
alheranki. Ke dai dabam ce, gama kikan biya kuma ba mai biyanki.
35 " 'Saboda haka, ke karuwa, ki ji maganar UBANGIJI! 36 Ga abin da UBANGIJI Mai
Iko Duka yana cewa domin kin zubar da dukiyarki* kika bayyana tsiraicinki cikin
fasikancinki da kwartayenki, kuma saboda dukan gumakan banƙyamarki, kuma
saboda kin ba su jinin 'ya'yansu, 37 saboda haka zan tattara dukan kwartayenki,
waɗanda kike jin daɗinsu, waɗanda kike ƙauna da waɗanda kike ƙi. Zan tattara su
gāba da ke daga dukan kewaye zan kuma tuɓe ki a gabansu, za su kuwa ga dukan
tsiraicinki. 38 Zan hukunta ki da hukuncin matan da suke zina da kuma waɗanda suke
zub da jini; zan kawo hakkin jini na fushina da kuma fushin kishina. 39 Sa'an nan zan
miƙa ki ga kwartayenki, za su kuwa rurrushe ɗakunan samanki su kuma farfashe
ɗakunan tsafinki. Za su tuɓe miki tufafinki su kuma kwashe kayan adonki masu
kyau su bar ki tsirara tik. 40 Za su kawo taron jama'a a kanki, waɗanda za su jajjefe
ki da dutse su sassare ki gunduwa-gunduwa da takubansu. 41 Za su ƙone gidajenki
su kuma hukunta ki a idon mata masu yawa. Zan kawo ƙarshen karuwancinki, ba
za ki kuma ƙara biyan kwartayenki ba. 42 Sa'an nan fushina a kanki zai huce fushin
kishina kuma ya kwanta; zan huce ba kuwa zan ƙara yin fushi ba.
43 " 'Domin ba ki tuna da kwanakin ƙuruciyarki ba amma kika husatar da ni da
waɗannan abubuwa, tabbatacce zan sāka miki alhakin ayyukanki, in ji UBANGIJI Mai
Iko Duka. Ba kin ƙara lalata ga dukan waɗansu ayyuka masu banƙyamarki ba?
44 " 'Duk mai yin amfani da karin magana zai faɗi wannan karin magana a kanki
cewa, "Kamar yadda mahaifiya take haka 'yar take." 45 Ke 'yar mahaifiyarki ce da
gaske, wadda ta ƙi mijinta da 'ya'yanta; ke kuma 'yar'uwar 'yar'uwanki mata ce
da gaske, waɗanda suka ƙi mazansu da 'ya'yansu. Mahaifiyarki mutuniyar Hitti
ce, mahaifinki kuma mutumin Amoriyawa ne. 46 Babbar 'yar'uwarki mutuniyar
Samariya ce, wadda take zaune da 'ya'yanta mata wajen arewa da ke; ƙanuwarki ita
ce Sodom wadda take zaune kudu da ke tare da 'ya'yanta mata. 47 Ba ki bi hanyoyinsu
da abubuwansu na banƙyama kaɗai ba, sai ka ce wannan ya yi miki kaɗan, amma
kin lalace fiye da su. 48 Muddin in raye, in ji UBANGIJI Mai Iko Duka, 'yar'uwarki
Sodom da 'ya'yanta mata ba su yi abin da 'ya'yanki mata suka yi ba.
49 " 'To, fa, ga zunubin 'yar'uwarki Sodom. Ita da 'ya'yanta mata sun yi girman kai,
sun ƙoshi fiye da kima kuma ba su kula da wani abu ba; ba su taimaki matalauta da
kuma masu bukata ba. 50 Su masu girman kai ne kuma suka aikata abubuwa masu
banƙyama a gabana. Saboda haka na kau da su kamar yadda ka gani. 51 Samariya
ba tă aikata ko rabin zunubanki ba. Kin aikata abubuwa masu banƙyama fiye da
su, suka kuma sa 'yan'uwanki mata suka zama kamar masu adalci ta wurin dukan

§ **16:29** Ko kuwa Kaldiya * **16:36** Ko kuwa sha'awar

waɗannan abubuwa da kika aikata. 52 Ki sha kunyarki, gama kin yi rangwame wa
ʼyanʼuwanki mata. Saboda zunubanki sun yi muni fiye da nasu, sai suka zama kamar
sun fi ki adalci. Saboda haka, ki sha kunya ki kuma sha ƙasƙancinki, gama kin sa
ʼyanʼuwanki mata suka zama kamar su masu adalci ne.
53 “ ‘Amma fa, zan komo da nasarar Sodom da ʼyaʼyanta mata da ta Samariya da
ʼyaʼyanta mata, nasararki kuma tare da su, 54 domin ki sha ƙasƙancinki ki kuma
sha kunyar dukan abin da kika aikata ta wurin taʼazantar da su. 55 ʼYanʼuwanki
kuwa, Sodom da ʼyaʼyanta mata da Samariya tare da ʼyaʼyanta mata, za su koma
kamar yadda suke a dā; ke kuma da ʼyaʼyanki mata za ku koma kamar yadda kike
a dā. 56 Ba za ki ma iya ambaci ʼyarʼuwarki Sodom a ranar fariyarki ba, 57 kafin
a tone muguntarki. Ko da ma haka, yanzu ʼyaʼyan Arameyawa mata da dukan
maƙwabtanta da kuma ʼyaʼyan Filistiyawa mata suna miki dariyar, dukan waɗanda
suke kewaye da ke da suka rena ki. 58 Za ki ɗauki hakkin lalatarki da kuma ayyukanki
masu banƙyama, in ji Ubangiji.
59 “ ‘Ga abin da Ubangiji Mai Iko Duka yana cewa zan hukunta kamar yadda ya dace
da ke, domin kin ƙyale rantsuwana ta wurin karya alkawari. 60 Duk da haka zan tuna
da alkawarin da na yi da ke a kwanakin ƙuruciyarki, zan kuma kafa madawwamin
alkawari da ke. 61 Saʼan nan za ki tuna da hanyoyinki ki kuma ji kunya saʼad da kika
karɓi ʼyanʼuwanki mata, waɗanda suka girme ki da kuma waɗanda kika girme su.
Zan ba da su kamar ʼyaʼya mata gare ki, amma ba bisa alkawarina da ke ba. 62 Ta
haka zan kafa alkawarina da ke, za ki kuma san cewa ni ne Ubangiji. 63 Saʼan nan,
saʼad da na yi kafara saboda ke domin dukan abin da kika aikata, za ki tuna ki kuma
ji kunya har ki kāsa buɗe bakinki saboda kunya, in ji Ubangiji Mai Iko Duka.’ ”

# 17

*Gaggafa biyu da kuringa guda*

1 Maganar Ubangiji ta zo mini cewa, 2 “Ɗan mutum, ka shirya kacici-kacici ka
faɗa wa gidan Israʼila misali. 3 Ka ce musu, ‘Ga abin da Ubangiji Mai Iko Duka yana
cewa babbar gaggafa mai manyan fikafikai, dogayen gasusuwa da gasusuwa da yawa
masu launi iri-iri ta zo Lebanon. Ta cire kan alʼul, 4 ta karya kan tohonsa da yake can
bisansa ta kai ƙasar ciniki, inda ta shuka shi a birnin ʼyan kasuwa.
5 “ ‘Ta ɗebi waɗansu irin ƙasarku ta sa a ƙasa mai taƙi. Ta shuka shi kamar itacen
wardi kusa da ruwa mai yawa, 6 ya kuwa yi toho ya zama kuringa gajeruwa mai
yaɗuwa. Rassanta suka tanƙwasa wajen gaggafar, amma saiwoyinta suka zauna a
ƙarƙashinta. Ta haka ta zama kuringa, ta yi rassa ta kuma fid da ganyaye.
7 “ ‘Akwai kuma wata babbar gaggafa mai manyan fikafikai da gashi mai yawa.
Kuringan nan ta tanƙwasa saiwoyinta zuwa wajen wannan gaggafa daga inda aka
shuka ta, ta kuma miƙe rassanta wajenta don gaggafar ta yi mata banruwa. 8 An
shuka ta a ƙasa mai kyau kusa da ruwa mai yawa don tă yi rassa masu yawa, ta ba
da ʼyaʼya ta kuma zama kuringa mai daraja.’
9 “Ka gaya musu cewa, ‘Ga abin da Ubangiji Mai Iko Duka yana cewa wannan za
tă ci gaba? Ba za a tumɓuke ta a kuma kakkaɓe ʼyaʼyanta don ta bushe ba? Dukan
sababbin tohonta za su bushe. Ba sai da hannu mai ƙarfi, ko kuwa da yawan mutane
za a tumɓuke ta daga saiwoyinta ba. 10 Ko da an sāke shuka ta, za tă yi amfani ne?
Ba za tă bushe gaba ɗaya saʼad da iskar gabas ta hura ba, tă bushe a ƙasar da ta yi
girma?’ ”
11 Sai maganar Ubangiji ta zo mini cewa, 12 “Ka faɗa wa gidan ʼyan tawayen nan,
‘Ba ka san abin da waɗannan abubuwa suke nufi ba?’ Ka faɗa musu cewa, ‘Sarkin
Babilon ya tafi Urushalima ya tafi da sarkinta da kuma manyan garinta, ya dawo
da su Babilon. 13 Saʼan nan ya ɗauki wani daga iyalin sarauta ya yi yarjejjeniya da

shi, ya sa shi ya yi rantsuwa. Ya kuma tafi da shugabannin ƙasar, 14 don a raunana
masarautar, kada tă ƙara tashi, amma ta tsaya dai kan cika yarjejjeniyarsa. 15 Amma
sarkin nan ya yi tawaye a kan sarkin Babilon ta wurin aika jakadunsa zuwa Masar
don a ba shi dawakai da sojoji masu yawa. Zai ci nasara? Shi da ya yi wannan abu
zai tsira? Zai iya taka yarjejjeniya har ya tsere?
16 " 'Muddin in raye, in ji UBANGIJI Mai Iko Duka, zai mutu a Babilon, a ƙasar sarkin
nan da ya naɗa shi, domin bai cika rantsuwa da alkawarin da ya yi ba. 17 Fir'auna
da yawan sojojinsa da kuma yawan jama'arsa ba zai zama da taimako gare shi a yaƙi
ba, sa'ad da sarkin Babilon zai gina mahaurai ya kuma yi ƙawanya don yă hallaka
rayuka masu yawa. 18 Bai cika rantsuwa ba ta wurin take alkawari. Domin sarkin
Isra'ila ya ƙulla alkawari ya kuma aikata dukan waɗannan abubuwa, ba zai tsira ba.
19 " 'Saboda haka ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka ya ce muddin ina raye, zan
nemi hakkin rantsuwata da ya ƙi cikawa da kuma alkawarin da ya take. 20 Zan kafa
masa tarkona, zai kuma fāɗi a tarkona. Zan kawo shi a Babilon in kuma hukunta shi
a can domin ya yi mini rashin aminci. 21 Dukan sojojinsa zaɓaɓɓu za a kashe su da
takobi, za a kuma watsar da waɗanda suka ragu ko'ina. Ta haka za ku san cewa Ni
UBANGIJI na faɗa.
22 " 'Ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa ni kaina zan cire toho a kan
itacen al'ul da yake can bisa in shuka; zan kuma karya ƙanƙanin reshe daga can
bisan tohon in shuka a dutse mai tsayi. 23 A ƙwanƙolin dutsen Isra'ila zan shuka
shi; zai yi rassa yă ba da 'ya'ya yă kuma zama al'ul mai daraja. Tsuntsaye iri-iri za
su yi sheƙa a cikinsa; za su sami mafaka a inuwar rassansa. 24 Dukan itatuwan jeji
za su san cewa Ni UBANGIJI ne mai sa manyan itatuwa su zama ƙanana in kuma sa
ƙananan itatuwa su zama manya. Nakan sa ɗanyen itace ya bushe, busasshen itace
kuma ya zama ɗanye.
" 'Ni UBANGIJI na faɗa, zan kuma aikata.' "

## 18

*Mutumin da ya yi zunubi zai mutu*

1 Maganar UBANGIJI ta zo mini cewa, 2 "Me ku mutane kuke nufi da faɗar wannan
karin magana a kan ƙasar Isra'ila cewa,
" 'Ubanni sun ci 'ya'yan inabi masu tsami,
haƙoran 'ya'ya kuwa sun mutu'?
3 "Muddin ina raye, in ji UBANGIJI Mai Iko Duka, ba za ku ƙara faɗar wannan karin
magana a Isra'ila ba. 4 Gama kowane mai rai nawa ne, mahaifi da ɗa, duk nawa ne.
Mutumin da ya yi zunubi shi zai mutu.
5 "A ce akwai mai adalci
wanda yake aikata abin da yake daidai da kuma gaskiya;
6 ba ya cin abinci a duwatsun tsafi
ko ya dogara ga gumakan gidan Isra'ila.
Ba ya ƙazantar da matar maƙwabcinsa
ko ya kwana da mace lokacin al'adarta ba.
7 Ba ya cin zalin wani,
amma yakan mayar wa wanda ya ba shi jingina abin da ya jinginar masa.
Ba ya yi fashi
amma yakan ba wa mayunwata abinci
ya kuma tanada wa marasa tufafi riga.
8 Ba ya ba da bashi da ruwa
ko ya karɓa ƙarin riba.*

* 18:8 Ko kuwa karɓi riba; yadda yake a ayoyi 13 da 17

Yakan janye hannunsa daga aikata mugunta
yakan kuma yi shari'a cikin gaskiya tsakanin mutum da mutum.
9 Yana bin ƙa'idodina
yana kuma kiyaye dokokina da aminci.
Wannan mutumin adali ne;
tabbatacce zai rayu,
in ji UBANGIJI Mai Iko Duka.
10 "A ce yana da ɗa wanda yana kisa ko yana yin ɗaya daga cikin waɗannan
abubuwa† 11 (ko da yake mahaifin bai yi ko ɗaya daga cikinsu ba).
"Yakan ci abinci a duwatsun tsafi.
Yakan ƙazantar da matar maƙwabci.
12 Yakan ci zalin matalauta da mabukata.
Yakan yi fashi.
Ba ya mayar da abin da aka jinginar masa.
Ya dogara ga gumaka.
Yana aikata ayyukan banƙyama.
13 Yakan ba da bashi da ruwa ya kuma karɓi riba mai yawa.
Irin wannan mutum zai rayu? Ba zai rayu ba! Domin ya aikata dukan waɗannan abubuwa masu banƙyama, tabbatacce za a kashe shi, kuma hakkin jininsa zai zauna a kansa.
14 "Amma a ce wannan ɗa yana da ɗa wanda ya ga dukan zunuban da mahaifinsa yake aikata, kuma ko da yake ya gan su, bai yi ko ɗaya daga cikin irin abubuwan nan ba, wato,
15 "Bai ci abinci a duwatsun tsafi ba
ko ya dogara ga gumakan gidan Isra'ila.
Bai ƙazantar da matar maƙwabcinsa ba.
16 Bai ci zalin wani
ko ya karɓi jingina ba.
Ba ya fashi
amma yakan ba da abincinsa ga mayunwata
ya tanada tufafi wa marasa tufafi.
17 Yakan janye hannunsa daga zunubi‡
ba ya kuma ba da bashi da ruwa ko karɓan riba da yawa.
Yakan kiyaye dokokina ya kuma bi ƙa'idodina.
Ba zai mutu saboda zunubin mahaifinsa ba; tabbatacce zai rayu. 18 Amma mahaifinsa
zai mutu saboda zunubinsa, domin ya yi ƙwace, ya yi wa ɗan'uwansa fashi ya kuma yi abin da ba daidai ba a cikin mutanensa.
19 "Duk da haka kukan yi tambaya, 'Me ya sa ɗan ba zai sami rabo a laifin mahaifinsa ba?' Da yake ɗan ya yi abin da yake daidai da kuma gaskiya, ya kuma kiyaye dukan ƙa'idodina, tabbatacce zai rayu. 20 Mutumin da ya yi zunubi shi zai
mutu. Ɗa ba zai sami rabo a laifin mahaifi ba, mahaifi ba zai sami rabo a laifi ɗa ba. Adalcin adali zai zama nasa, muguntar mugu za tă koma kansa.
21 "Amma in mugun mutum ya juya daga dukan zunubin da ya aikata ya kuma kiyaye dukan ƙa'idodina ya kuwa yi abin da yake daidai da kuma gaskiya, tabbatacce zai rayu; ba zai mutu ba. 22 Babu laifin da ya yi da za a tuna da su. Saboda abubuwan
adalcin da ya aikata, zai rayu. 23 Ina jin daɗin mutuwar mugu ne? In ji UBANGIJI Mai Iko Duka. A maimako, ban fi jin daɗi sa'ad da suka juyo daga hanyoyinsu suka rayu ba?
24 "Amma in mai adalci ya juya daga adalcinsa ya yi zunubi ya kuma aikata abubuwa masu banƙyamar da mugun mutum ke aikatawa, zai rayu? Babu

† 18:10 Ko kuwa abubuwa ga ɗan'uwa ‡ 18:17 Seftuwajin (duba kuma aya 8); Ibraniyanci daga matalauta

abubuwan adalcin da ya aikata da za a tuna da su. Saboda rashin amincinsa da
kuma saboda zunubai da ya yi, zai mutu.
25 “Duk da haka kun ce, ‘Hanyar Ubangiji ba daidai ba ce.’ Ka ji, ya gidan Isra’ila.
Hanyata ba daidai ba ce? 26 In mai adalci ya juye daga adalcinsa ya yi zunubi,
zai mutu saboda wannan; saboda zunubin da ya yi, zai mutu. 27 Amma in mugun
mutum ya juye daga muguntarsa ya kuma yi abin da yake daidai da kuma gaskiya,
zai ceci ransa. 28 Domin ya lura da dukan laifofin da ya yi ya kuma juye daga gare
su, tabbatacce zai rayu; ba zai mutu ba. 29 Duk da haka mutanen Isra’ila sun ce,
‘Hanyar Ubangiji ba daidai ba ce.’ Hanyoyina ba daidai ba ne, ya gidan Isra’ila? Ba
hanyoyinku ne ba daidai ba?
30 “Saboda haka, ya gidan Isra’ila, zan hukunta ku, kowa bisa ga hanyarsa, in ji
UBANGIJI Mai Iko Duka. Ku tuba! Ku juye daga dukan laifofinku; sa’an nan zunubi ba
zai zama sanadin fāɗuwarku ba. 31 Ku raba kanku da dukan laifofin da kuka yi, ku
sami sabuwar zuciya da sabon ruhu. Don me za ku mutu, ya gidan Isra’ila? 32 Gama
ba na jin daɗin mutuwar wani, in ji UBANGIJI Mai Iko Duka. Ku tuba don ku rayu!

# 19

### *Makoki domin sarakunan Isra’ila*

1 “Ka yi makoki game da sarakunan Isra’ila 2 ka ce,
“ ‘Mahaifiyarki zakanya ce
cikin zakoki!
Takan kwanta cikin ’yan zakoki
ta kuma yi renon kwiyakwiyanta.
3 Ta goyi ɗaya daga cikin kwiyakwiyanta,
ya yi girma ya zama zaki mai ƙarfi.
Ya koyi yayyage abin da ya yi farauta
yakan kuma cinye mutane.
4 Al’ummai suka ji labarinsa,
aka kuma kama shi cikin raminsu.
Suka ja shi da ƙugiyoyi
zuwa ƙasar Masar.

5 “ ‘Sa’ad da ta ga sa zuciyarta bai cika ba,
abin da take fata gani ya tafi,
sai ta ɗauki wani daga cikin kwiyakwiyanta
ta mai da shi zaki mai ƙarfi.
6 Ya yi ta yawo a cikin zakoki,
gama yanzu shi zaki ne mai ƙarfi.
Ya koyi yayyage abin da ya yi farauta
yakan kuma cinye mutane.
7 Ya rurrushe kagaransu
ya kuma ragargaza biranensu.
Kasar da dukan waɗanda suke cikinta
sun tsorata da jin rurinsa.
8 Sai al’ummai suka tayar masa,
waɗannan daga yankunan da suke kewaye.
Suka yafa raga dominsa
ya kuwa fāɗa cikin raminsu.
9 Da ƙugiyoyi suka ja shi cikin keji
suka kawo shi wurin sarkin Babilon.
Suka sa shi cikin kurkuku,

saboda haka ba a ƙara jin rurinsa
a kan duwatsun Isra'ila ba.

10 " 'Mahaifiyarku kamar kuringa ce a cikin gonar inabi
da aka shuka kusa da ruwa;
ta ba da 'ya'ya da kuma cikakkun rassa
saboda yalwan ruwa.
11 Rassanta suka yi ƙarfi,
suka dace da sandar mai mulki.
Ta yi tsayi
zuwa sama
ana ganin ta saboda tsayinta
da kuma saboda yawan rassanta.
12 Amma aka tumɓuke ta cikin fushi
aka jefar da ita a ƙasa.
Iskar gabas ta sa ta yanƙwane,
aka kakkaɓe 'ya'yanta;
rassanta masu ƙarfi suka bushe
wuta kuma ta cinye su.
13 Yanzu an shuka ta a hamada,
a busasshiyar ƙasa marar ruwa.
14 Wuta ta fito daga jikin rassanta
ta cinye 'ya'yanta.
Babu sauran reshe mai ƙarfin da ya rage a kanta
da ya dace da sandar mai mulki.'
Wannan waƙa ce kuma za a yi amfani da ita a matsayin makoki."

# 20

*Isra'ila 'yan tawaye*

1 A shekara ta bakwai, a wata na biyar a rana ta goma, waɗansu dattawan Isra'ila
suka zo don su nemi nufin UBANGIJI, suka kuwa zauna a ƙasa a gabana.
2 Sai maganar UBANGIJI ta zo mini cewa, 3 "Dan mutum, ka yi magana da dattawan
Isra'ila ka ce musu, 'Ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa kun zo ne ku nemi
shawarata? Muddin ina raye, ba zan bari ku nemi shawarata ba, in ji UBANGIJI Mai
Iko Duka.'
4 "Za ka hukunta su? Za ka hukunta su, ɗan mutum? To, sai ka kalubalance su da
ayyukan banƙyamar kakanninsu 5 ka ce musu, 'Ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka
yana cewa a ranar da na zaɓi Isra'ila, na ɗaga hannuna, na rantse wa zuriyar gidan
Yaƙub na kuma bayyana kaina gare su a Masar da hannun da na ɗaga na ce musu,
"Ni ne UBANGIJI Allahnku." 6 A ranar na yi musu rantsuwa cewa zan fitar da su daga
Masar zuwa ƙasar da na samo musu, ƙasa mai zub da madara da zuma, ƙasa mafi
kyau cikin dukan ƙasashe. 7 Na kuma ce musu, "Kowannenku ya zubar da mugayen
siffofin da kuka kafa idanunku a kai, kuma kada ku ƙazantar da kanku da gumakan
Masar. Ni ne UBANGIJI Allahnku."
8 " 'Amma sai suka yi tawaye a kaina ba su kuwa saurare ni ba; ba su zubar da
mugayen siffofin da suka kafa idanunsu a kai ba, balle su ƙi gumakan Masar. Saboda
haka zan zubo hasalata a kansu in kuma aukar musu da fushina a Masar. 9 Amma
saboda sunana na yi abin da zai kiyaye shi daga ƙazantuwa a idanun al'umman da
suka zauna a ciki da kuma a idanun al'ummai da na bayyana kaina ga Isra'ilawa
ta wurin fitar da su daga Masar. 10 Saboda haka na fisshe su daga Masar na kawo
su cikin hamada. 11 Na ba su ƙa'idodina na kuma sanar musu da dokokina, gama

mutumin da ya yi biyayya da su zai rayu ta wurinsu. 12 Na kuma ba su Asabbataina
kamar alama tsakaninmu, domin su san cewa Ni UBANGIJI ne yake tsarkake su.
13 " 'Duk da haka mutanen Isra'ila suka yi mini tawaye a cikin hamada. Ba su bi
ƙa'idodina ba amma suka ki dokokina, ko da yake mutumin da ya yi biyayya da su zai
rayu ta wurinsu, suka ɓata Asabbataina ƙwarai. Saboda haka na ce zan zuba hasalata
a kansu in kuma hallaka su a hamada. 14 Amma saboda sunana na yi abin da zai
kiyaye shi daga ƙazantuwa a idanun al'umman da a idonsu na fisshe su. 15 Na kuma
ɗaga hannu na rantse musu a hamada cewa ba zan kawo su ƙasar da na ba su ba,
ƙasa mai zub da madara da zuma, ƙasa mafi kyau cikin dukan ƙasashe, 16 domin sun
ƙi dokokina ba su kuwa bi ƙa'idodina ba suka kuma ƙazantar da Asabbataina. Gama
zukatansu sun fi so su bauta wa gumakansu. 17 Duk da haka na dube su ta tausayi
ba zan hallaka su ko in kawo ƙarshensu a hamada ba. 18 Na faɗa wa 'ya'yansu a
hamada, "Kada ku bi farillai kakanninku ko ku kiyaye dokokinsu ko ku ƙazantar da
kanku da gumakansu. 19 Ni ne UBANGIJI Allahnku; ku bi ƙa'idodina ku kuma kula ku
kiyaye dokokina. 20 Ku kiyaye Asabbataina da tsarki, don su zama alama tsakaninmu.
Ta haka za ku san cewa ni ne UBANGIJI Allahnku."
21 " 'Amma 'ya'yan suka yi mini tawaye. Ba su bi ƙa'idodina ba, ba su kula su
kiyaye dokokina ba, ko da yake mutumin da ya kiyaye su zai rayu ta wurinsu, suka
kuma ƙazantar da Asabbataina. Saboda haka na ce zan zuba hasalata a kansu in
kuma aukar musu da fushina a hamada. 22 Amma na janye hannuna, kuma saboda
sunana na yi abin da zai kiyaye shi daga ƙazantuwa a idanun al'umman da a idonsu
na fisshe su. 23 Na kuma ɗaga hannu na rantse musu cewa zan watsar da su cikin
al'ummai in kuma warwatsa su cikin ƙasashe, 24 domin ba su kiyaye dokokina ba
amma suka ƙi ƙa'idodina suka kuma ƙazantar da Asabbataina, idanunsu suka yi
sha'awar gumakan kakanninsu. 25 Na kuma ba da su ga farillan da ba su da kyau da
dokokin da ba za su rayu ta wurinsu ba; 26 na bari suka ƙazantu ta wurin kyautai,
hadayar kowane ɗan fari* don in cika su da abin tsoro domin su san cewa ni ne
UBANGIJI.'
27 "Saboda haka, ɗan mutum, ka yi magana da mutanen Isra'ila ka faɗa musu cewa,
'Ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa a wannan kuma kakanninku suka saɓe
ni ta wurin yashe ni. 28 Sa'ad da na kawo su cikin ƙasar da na rantse zan ba su suka
kuma ga tudu mai tsawo ko itace mai ganye, a can suka miƙa hadayunsu, suka yi
sadakokin da suka tsokane ni na yi fushi, suka miƙa turaren ƙanshinsu suka kuma
zuba sadakokinsu na sha. 29 Sai na ce musu, Wane ɗakin tsafi kuke tafiya?' " (Ana ce
da shi Bama† har wa yau.)

### *Hukunci da Maidowa*

30 "Domin haka ka faɗa wa gidan Isra'ila, 'Ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana
cewa za ku ƙazantar da kanku yadda kakanninku suka yi ne ku yi sha'awar mugayen
siffofinsu? 31 Sa'ad da kuka miƙa kyautai naku, hadayar 'ya'yanku maza a‡ wuta,
kuna cin gaba da ƙazantar da kanku da duka gumakanku har wa yau. Zan bari ku
nemi shawarata, ya gidan Isra'ila? Muddin ina raye, in ji UBANGIJI Mai Iko Duka, ba
zan bari ku nemi shawarata ba.
32 " 'Kukan ce, "Kuna so ku zama kamar sauran al'ummai, kamar sauran mutanen
duniya, waɗanda suke bauta wa itace da dutse." Amma abin da kuke tunani ba zai
taɓa faruwa ba. 33 Muddin ina raye, in ji UBANGIJI Mai Iko Duka, zan yi mulki a kanku
da hannu mai iko da kuma hannu mai ƙarfi da kuma fushi. 34 Zan fitar da ku daga
al'ummai in tattara ku daga ƙasashe inda aka warwatsa ku, da hannu mai iko da
kuma hannu mai ƙarfi da kuma fushi. 35 Zan kawo ku cikin hamadar al'ummai a can

* **20:26** Ko kuwa sa kowane ɗan fari ya ratsa wuta † **20:29** Bama yana nufin masujadar kan tudu. ‡ **20:31** Ko kuwa kuna sa 'ya'yanku maza su ratsa ciki

kuwa, fuska da fuska, zan hukunta ku. 36 Yadda na hukunta kakanninku a hamadar
ƙasar Masar, haka zan hukunta ku, in ji UBANGIJI Mai Iko Duka. 37 Zan lura da ku
yayinda kuke wucewa ƙarƙashin sanda, zan kuma kawo ku cikin daurin alkawari.
38 Zan fitar da waɗanda suke mini tayarwa da kuma ’yan tawaye. Ko da yake zan
fitar da su daga ƙasar da suke zama, duk da haka ba za su shiga ƙasar Isra’ila ba.
Sa’an nan za ku san cewa ni ne UBANGIJI.
39 “ ‘Game da ku, ya gidan Isra’ila, ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa
ku tafi ku bauta wa gumakanku, kowannenku! Amma daga baya tabbatacce za ku
saurare ni ba kuwa za ku ƙara ɓata sunana mai tsarki da hadayunku da gumakanku
ba. 40 Gama a kan dutsena mai tsarki, dutse mai tsayi na Isra’ila, in ji UBANGIJI Mai
Iko Duka, a can a ƙasar gidan Isra’ila gaba ɗaya za su bauta mini, a can kuwa zan
karɓe su. A can zan bukaci hadayunku da sadake sadakenku mafi kyau,§ tare da
dukan tsarkakan hadayunku. 41 Zan karɓe ku kamar turare mai ƙanshi sa’ad da
na fitar da ku daga al’ummai na kuma tattara ku daga ƙasashe inda aka warwatsa
ku, zan kuma nuna kaina mai tsarki a cikinku a idon al’ummai. 42 Sa’an nan za ku
san cewa ni ne UBANGIJI sa’ad da na kawo ku cikin ƙasar Isra’ila, ƙasar da na ɗaga
hannu na rantse zan ba wa kakanninku. 43 A can za ku tuna da halinku da kuma
dukan ayyukanku waɗanda kuka ɓata kanku da su, za ku kuwa ji ƙyamar kanku
saboda mugayen abubuwan da kuka aikata. 44 Za ku san cewa ni ne UBANGIJI, sa’ad
da na yi muku haka saboda sunana ba bisa ga mugayen hanyoyinku da ayyukanku
marasa kyau ba, ya gidan Isra’ila, in ji UBANGIJI Mai Iko Duka.’ ”

*Annabci a kan kudu*

45 Maganar UBANGIJI ta zo mini cewa, 46 “Dan mutum, ka kafa fuskarka wajen kudu;
ka yi wa’azi a kan kudu ka kuma yi annabci a kan kurmin ƙasar kudu. 47 Ka faɗa
wa kurmin kudanci, ‘Ji maganar UBANGIJI. Ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana
cewa ina gab da sa maka wuta, za tă kuwa cinye dukan itatuwanki sarai, da ɗanye
da busasshe. Ba za a kashe wutar da take ci ba, kuma kowace fuska a kudu zuwa
arewa za tă ƙone. 48 Kowa zai san cewa Ni UBANGIJI ne ya ƙuna ta; ba za a kashe ta
ba.’ ”
49 Sai na ce, “Kash, UBANGIJI Mai Iko Duka! Suna zance a kaina cewa, ‘Ba misalai
kawai yake yi ba?’ ”

# 21

*Babilon, takobin hukuncin Allah*

1 Maganar UBANGIJI ta zo mini cewa, 2 “Dan mutum, ka kafa fuskarka gāba da
Urushalima ka kuma yi wa’azi a kan wuri mai tsarki. Ka yi annabci gāba da ƙasar
Isra’ila 3 ka faɗa mata, ‘Ga abin da UBANGIJI ya ce ina gāba da ke. Zan ja takobina
daga kubensa in karkashe adalai da mugaye daga cikinki. 4 Domin zan karkashe
adalai da kuma mugaye, ba zan rufe takobina a kan kowa daga kudu zuwa arewa ba.
5 Sa’an nan duka mutane za su san cewa Ni UBANGIJI na ja takobina daga kubensa;
ba zai sāke koma kuma ba.’
6 “Saboda ka yi nishi, ɗan mutum! Yi nishi a gabansu da ajiyar zuciya da ɓacin
rai. 7 Kuma sa’ad da suka tambaye ka, ‘Me ya sa kake nishi?’ Sai ka ce musu, ‘Domin
labarun da suke fitowa. Kowace zuciya za tă narke kowane hannu kuma ya gurgunta;
kowane ruhu zai sume kowane gwiwa kuma ta rasa ƙarfi kamar ruwa.’ Yana zuwa!
Tabbatacce zai faru, in ji UBANGIJI Mai Iko Duka.”
8 Maganar UBANGIJI ta zo mini cewa, 9 “Dan mutum, yi annabci ka ce, ‘Ga abin da
Ubangiji ya faɗa,
“ ‘Takobi, takobi,

§ **20:40** Ko kuwa da kyautai ’ya’yan farinku

wasasshe da kuma gogagge,
10 wasasshe don kisa,
gogagge har yana walwal kamar walƙiya!
“ ‘Kada ku yi farin ciki, hukunci yana zuwa, domin kowa ya ƙi jin abin da na yi
gargaɗi a kai.
11 “ ‘An ba da wannan takobi don a goge,
don a kama da hannu;
an washe shi aka kuma goge,
shiryayye don a yi kisa da shi.
12 Ka yi kuka ka yi makoki, ɗan mutum,
gama yana gāba da dukan sarakunan Isra’ila.
An jefa su ga takobi
tare da jama’ata.
Saboda haka ku buga ƙirjinku.
13 “ ‘Gwaji tabbatacce zai zo. Kuma a ce sandan Yahuda, wanda takobi ya ƙi, ya ci
gaba? In ji UBANGIJI Mai Iko Duka.’
14 “Saboda haka fa, ɗan mutum ka yi annabci
ka kuma tafa hannuwanka.
Bari takobi ya yi sara sau biyu,
har sau uku ma.
Takobin kisa ne,
takobi ne don kisa mai girma,
zai kewaye su a kowane gefe.
15 Domin zukata su narke
da yawa kuma su fāɗi,
na tsai da takobin kisa
a dukan ƙofofinsu.
Kash! A sa ya haska kamar walƙiya,
ana riƙe da shi don kisa.
16 Ya takobi, yi sara zuwa dama
ka yi kuma zuwa hagu,
duk inda aka juya ka.
17 Zan tafa hannuwana,
fushina kuwa zai sauka.
Ni UBANGIJI na faɗa.”
18 Sai maganar UBANGIJI ta zo mini cewa, 19 “Dan mutum, ka nuna hanyoyi biyu inda
takobin sarkin Babilon zai bi, duka biyun su fara daga ƙasa guda. Ka kafa shaida inda
hanyar za tă rabu zuwa cikin birni. 20 Ka nuna hanya guda wadda takobi zai fāɗo wa
Rabba ta Ammonawa ɗayan kuma da zai fāɗo a kan Yahuda da kuma Urushalima mai
katanga. 21 Gama sarkin Babilon zai tsaya a mararrabar hanya, a inda hanyar ta rabu
biyu, don yă yi duba. Zai jefa ƙuri’a da kibiyoyinsa, zai nemi shawarar gumakansa,
zai bincike hanta. 22 A hannunsa na dama ƙuri’a don Urushalima za tă fito, inda zai
kafa dundurusai, ya ba da umarni kisa, a yi kururuwar yaƙi, a kafa dundurusai a
kan ƙofofi, a gina mahaurai a kuma yi ƙawanya. 23 Zai zama kamar duban ƙarya
ne ga waɗanda suka yi rantsuwar yin masa biyayya, amma zai tunashe su game da
laifinsu ya kuma kama su.
24 “Saboda haka ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa, ‘Domin ku mutanen
nan kun tuna da laifinku ta wurin tawaye, kun kuma bayyana zunubanku cikin dukan
abin da kuke yi, domin kun yi haka, za a kama ku.
25 “ ‘Ya kai ƙazantaccen mugu, yerima Isra’ila, wanda kwanansa ta zo, wanda
lokacin hukuncinsa ya cika fal, 26 ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa ka
kunce rawanin, ka ɗauke rawanin nan. Ba zai zama kamar yadda yake ba. Za a

ɗaukaka ƙasƙantacce, amma a ƙasƙantar da mai girma. 27 Hallaka! Hallaka! Zan
hallaka shi! Ba za a maido da shi ba sai ya ga ainihin mai shi; gare shi zan bayar da
shi.'

28 "Kai kuma, ɗan mutum, ka yi annabci ka ce, 'Ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka
yana cewa game da Ammonawa da kuma zarginsu.

" 'Takobi, takobi,
an ja don kisa,
an goge don cinyewa
yana haske kamar walƙiya!
29 Duk da wahayin ƙarya game da kai,
duban ƙarya game da kai,
za a sa shi a wuyan
mugaye waɗanda za a kashe,
waɗanda kwanansu ta zo,
waɗanda lokacin hukuncinsu ya cika fal.

30 " 'Ka mai da takobi a kubensa.
A inda aka halicce ka,
a ƙasar kakanninka,
zan hukunta ka.
31 Zan zub da hasalata a kanka
in hura maka wutar fushina;
Zan ba da kai a hannun mugayen mutanen
da suka gwanince a hallakarwa.
32 Za ka zama itacen wuta,
za a zub da jininka a ƙasarka,
ba za a ƙara tuna da kai ba;
gama Ni UBANGIJI na faɗa.' "

# 22

*Zunubin Urushalima*

1 Maganar UBANGIJI ta zo mini cewa,

2 "Dan mutum, za ka shari'anta ta? Za ka shari'anta wannan birni mai kisankai?
To, sai ka kalubalance ta da dukan ayyukanta na banƙyama 3 ka kuma ce, 'Ga abin
da UBANGIJI Mai Iko Duka ya ce ya birnin da take kawo wa kansa hallaka ta wurin
kisankai a cikinta kina kuma ƙazantar da kanki ta wurin yin gumaka, 4 kin zama mai
laifi saboda jinin da kika zubar kika kuma zama ƙazantacciya ta wurin gumakan
da kika yi. Kin kawo kwanakinki ga ƙarshe, kuma ƙarshen shekarunki sun zo.
Saboda haka zan mai da ke abar ba'a ga al'ummai da abin dariya ga dukan ƙasashe.
5 Waɗanda suke kusa da waɗanda suke nesa za su yi miki ba'a, ya ke birni marar
kunya, cike da rigima.

6 " 'Duba yadda kowane yerima Isra'ila waɗanda suke cikinki yake yin amfani da
ikonsa yana kisankai. 7 A cikinki sun rena mahaifi da mahaifiya; a cikinki sun zalunci
baƙo suka wulaƙanta maraya da gwauruwa. 8 Kin rena abubuwana masu tsarki kika
kuma ƙazantar da Asabbataina. 9 A cikinki akwai mutane waɗanda suka nace su yi
kisankai; a cikinki akwai waɗanda suke ci a dutsen tsafi suna yin ayyukan lalata. 10 A
cikinki akwai waɗanda suke kwana da matan mahaifansu; a cikinki akwai waɗanda
suke kwana da mata a lokacin da suke al'adarsu, sa'ad da suke da rashin tsarki. 11 A
cikinki mutum guda yakan yi laifi abin ƙyama da matar maƙwabcinsa, wani cikin
rashin kunya ya ƙazantar da matar ɗansa, wani kuma ya kwana da 'yar'uwansa, 'yar

mahaifinsa. 12 A cikinki mutane suna karɓan cin hanci don su yi kisankai; kina ba
da rance da ruwa da ƙari, kina kuma cin riba a kan maƙwabcinki ta wurin ƙwace.
Kina kuma manta da ni, in ji UBANGIJI Mai Iko Duka.
13 " 'Tabbatacce zan tafa hannuwana a kan ƙazamar riba da kika ci da jinin da kin
zubar a cikinki. 14 Karfin halinki zai jure ko kuwa hannuwanki za su yi ƙarfi a ranar
da na gamu da ke? Ni UBANGIJI na faɗa, zan kuma aikata. 15 Zan watsar da ke cikin
al'ummai in warwatsa ke cikin ƙasashe; zan kuma kawo ƙarshen rashin tsarkinki.
16 Sa'ad da ki ƙazantu* a idanun al'umma, za ki san cewa ni ne UBANGIJI.' "
17 Sai maganar UBANGIJI ta zo mini cewa, 18 "Ɗan mutum, gidan Isra'ila ta zama
ƙwan maƙera a gare ni; dukansu tagulla ne, kuza, ƙarfe da darma da suka rage a
tanderu. Su ƙwan maƙerar azurfa ne kawai. 19 Saboda haka ga abin da UBANGIJI
Mai Iko Duka yana cewa, 'Domin ku duka kun zama ƙwan maƙera, zan tattara ku a
Urushalima. 20 Kamar yadda mutane sukan tattara azurfa, tagulla, ƙarfe, darma da
kuza a cikin tanderu don su narkar da su da wuta, haka zan tattara ku cikin fushina
da kuma hasalata in sa ku cikin birnin in narkar da ku. 21 Zan tattara ku zan kuma
hura muku wutar hasalata, za ku kuma narke a cikinta. 22 Kamar yadda azurfa kan
narke a tanderu, haka za ku narke a cikinta, kuma za ku san cewa Ni UBANGIJI na
zubo muku da zafin fushina.' "
23 Har yanzu maganar UBANGIJI ta zo gare ni cewa, 24 "Ɗan mutum, ka faɗa
wa ƙasar, 'Ke ƙasa ce marar ruwan sama ko yayyafi a ranar hasala.' 25 Akwai
haɗin bakin sarakunanki a cikinki kamar rurin zaki mai yayyage ganimarsa; suna
cin mutane, suna kwashe dukiya da abububuwa masu daraja suna mai da yawanci
gwauraye a cikinki. 26 Firistocinki suna karya dokokina, sun ƙazantar da tsarkakan
abubuwana; ba sa bambanta tsakanin tsarki da marar tsarki; suna koyarwa cewa
babu bambanci tsakanin marar tsarki da mai tsarki; suna kuma rufe idanunsu ga
kiyaye Asabbataina, da haka suke saɓon sunana. 27 Shugabanninki a cikinki suna
kama da kyarketai masu yayyage ganimarsu; suna kisa suna kuma kashe mutane
don samun ƙazamar riba. 28 Annabawanki sun yi wa waɗannan ayyuka shafe da
farar ƙasa ta wurin wahayin ƙarya da duban ƙarya. Suna cewa, 'Ga abin da UBANGIJI
Mai Iko Duka yana cewa' alhali kuwa UBANGIJI bai faɗa ba. 29 Mutanen ƙasar na yin
ƙwace suna yin fashi; suna cin zalin matalauta da mabukata suna wulaƙanta baƙo
suna hana musu adalci.
30 "Na nemi mutum guda a cikinsu wanda zai gina katanga ya tsaya a gabana
a tsakani a madadin ƙasar don kada in hallaka ta, amma ban sami ko ɗaya ba.
31 Saboda haka zan zuba hasalata a kansu in cinye su da wutar fushina, ina ɗora
alhakin ayyukansu a bisa kawunansu, in ji UBANGIJI Mai Iko Duka."

# 23

*'Yan mata biyu mazinata*

1 Maganar UBANGIJI ta zo mini cewa, 2 "Ɗan mutum, an yi mata biyu, 'yan
matan mahaifiya guda. 3 Suka zama karuwai a Masar, suka yi karuwanci tun daga
ƙuruciyarsu. A wancan ƙasar an rungumi mamansu da ƙirjinsu na budurwanci.
4 Sunan babbar Ohola, ƙanuwarta kuwa Oholiba. Sun zama nawa suka kuma haifi
'ya'ya maza da mata. Ohola ita ce Samariya, Oholiba kuwa ita ce Urushalima.
5 "Ohola ta shiga karuwanci yayinda take zamana; ta kuwa yi ta kai da kawowa da
kwartayenta, Assuriyawa, mayaƙa 6 waɗanda suke saye da shunayya, gwamnoni da
manyan sojoji, dukansu samari ne masu bansha'awa, suna bisa kan dawakai. 7 Ta
ba da kanta ga duk waɗanda suke masu ilimin Assuriya ta kuma ƙazantar da kanta
da dukan gumaka na kowa da take kai da kawowa a cikinsu. 8 Ba ta bar karuwancin

* **22:16** Ko kuwa Sa'ad da na raba ki da gādonki

da ta fara a Masar ba, sa'ad da take budurwa maza sun kwana da ita, suka rungumi
ƙirjinta suka kuma biya kwaɗayinsu a kanta.
9 "Saboda haka na bashe ta ga kwartayenta, Assuriyawa, waɗanda ta yi ta kai da
kawowa a cikinsu. 10 Suka tuɓe ta tsirara, suka kwashe 'ya'yanta maza da mata suka
kuma kashe ta da takobi. Ta kuwa zama abin karin magana a cikin mata, aka kuma
yi mata hukunci.
11 "Kanuwarta Oholiba kuwa ta ga wannan, duk da haka cikin kai da kawowarta
da karuwancinta ta fi 'yar'uwar lalacewa. 12 Ita ma ta yi ta kai da kawowa cikin
Assuriyawa, gwamnoni da manyan sojoji; mayaƙa masu saye da kayan yaƙi, suna
bisa dawakai, dukansu samari ne masu bansha'awa. 13 Na ga cewa ita ma ta ƙazantar
da kanta; dukansu biyu sun bi hanya guda.
14 "Amma karuwancinta ya zarce. Ta ga an zāna mutane a kan bango, siffofin
sojojin Kaldiyawa* suna cikin jajjayen riguna, 15 da ɗamara a gindinsu da rawuna
a kansu suna kaɗawa falfal; dukansu sun yi kamar jarumawan kekunan yaƙin
Babiloniyawa 'yan Kaldiya.† 16 Nan da nan da ta gan su, sai ta yi sha'awarsu ta
aika da 'yan aika zuwa wurinsu a Kaldiya. 17 Sai Babiloniyawan suka zo wurinta,
zuwa gadon soyayya, cikin kai da kawowarsu suka ƙazantar da ita. Bayan sun
ƙazantar da ita, sai ta ji ƙyamarsu, ta rabu da su. 18 Sa'ad da ta ci gaba da yin
karuwancinta a fili ta kuma nuna tsiraicinta, sai na ji ƙyamarta, na rabu da ita,
kamar dai yadda na rabu da 'yar'uwarta. 19 Duk da haka sai ta yi ta ƙara fasikanci
tana tuna da kwanakin budurcinta, sa'ad da take karuwa a Masar. 20 A can ta yi ta
kai da kawowa da kwartayenta, waɗanda al'auransu kamar na jakuna ne waɗanda
maniyyinsu kuwa kamar na dawakai ne. 21 Haka kika yi ta lalacin budurcinki, sa'ad
da a Masar aka rungumi ƙirjinta aka tattaɓa nononta.‡
22 "Saboda haka, Oholiba, ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa zan
zuga kwartayenki su yi gāba da ke, su waɗanda kika ji ƙyamarsu, zan kuma
kawo su su yi gāba da ke daga kowane gefe, 23 Babiloniyawa da dukan Kaldiyawa,
mutanen Fekod da Showa da Kowa, da dukan Assuriyawa, samari masu bansha'awa,
dukan gwamnoni da manyan sojoji, hafsoshin keken yaƙin da mutane masu manyan
matsayi, dukansu a bisa dawakai. 24 Za su yi gāba da ke da kayan yaƙi,§ kekunan
yaƙi da kekunan doki da mutane masu yawa; za su ja dāgā a kanki a kowane gefe
da garkuwoyi manya da ƙanana da kuma hulunan kwano. Zan miƙa ke gare su don
hukunci, za su kuma hukunta ki bisa ga shari'arsu. 25 Zan nuna fushin kishina a
kanki, za su kuwa wulaƙanta ki da fushi. Za su yanke hancinki da kunnuwanki,
waɗanda suka rage miki kuma za a kashe su da takobi. Za su kama 'ya'yanki maza
da mata, waɗanda suka rage miki kuwa za a ƙone su da wuta. 26 Za su tuɓe tufafinki
su kuma kwashe kayan adonki masu kyau. 27 Ta haka zan tsai da marmari da kuma
karuwancin da kika fara a Masar. Ba za ki dubi waɗannan abubuwa da marmari ko
ki ƙara tuna da Masar ba.
28 "Gama ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa ina shirin miƙa ki ga
waɗanda suke ƙinki, ga waɗanda kika ji ƙyamarsu kika rabu da su. 29 Za su hukunta
ki da ƙiyayya su kuma kwashe kome da kika yi wahalarsa. Za su bar ki tsirara tik,
kunyan karuwancinki kuma zai tonu. Marmarinki da fasikancinki 30 sun jawo miki
wannan, domin ki yi ta kai da kawowa cikin ƙasashe kina ƙazantar da kanki da
gumakansu. 31 Kin bi hanyar 'yar'uwarki; saboda haka zan sa kwaf nata a hannunki.
32 "Ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa,
"Za ki sha kwaf na 'yar'uwarki,

* **23:14** Ko kuwa Babiloniyawa † **23:15** Ko kuwa Babiloniya; haka ma a aya 16 ‡ **23:21** Siriyak (dubi kuma 3); Ibraniyanci runguma saboda mamanki da suka fita sabo § **23:24** Ma'anar Ibraniyanci na wannan kalma babu tabbas.

kwaf wanda yake da girma da kuma zurfi;
zai jawo dariya da kuma reni
gama yana ɗauke da abubuwa da yawa.
33 Za ki cika da buguwa da baƙin ciki,
kwaf lalaci da kaɗaici,
kwaf na ʼyarʼuwarki Samariya.
34 Za ki sha shi ki kuma lashe shi ƙaf;
za ki buga shi da ƙasa ya yi rugu-rugu
ki tsattsage nononki.
Ni Ubangiji Mai Iko Duka na faɗa.

35 "Saboda haka ga abin da Ubangiji Mai Iko Duka yana cewa da yake kin manta
da ni kika tura ni bayanki, dole ki sha sakamakon marmarinki da karuwancinki."
36 Ubangiji ya ce mini, "Dan mutum, za ka shariʼanta Ohola da Oholiba? To, sai
ka kalubalance su da ayyukansu masu banƙyama, 37 gama sun yi zina kuma jinin
yana a hannuwansu. Sun yi zina da gumakansu; har suka miƙa ʼyaʼyansu da suka
haifa mini,* su zama musu abinci. 38 Sun kuma yi mini wannan. A lokaci guda
sun ƙazantar da wuri mai tsarkina suka ɓata Asabbataina. 39 A ranar da suka miƙa
ʼyaʼyansu ga gumakansu, sai suka shiga wuri mai tsarkina suka kuma ƙazantar da
shi. Abin da suka yi a gidana ke nan.
40 "Sun ma aiki manzanni wa mutanen da suka zo daga nesa, kuma da suka iso
kun yi wanka dominsu, kuka yi shafe-shafen idanunku, kuka kuma sa kayan adonku.
41 Kuka zauna a gado mai daraja, da tebur a shirye a gabanku wanda kun ajiye turare
da maina.
42 "Surutun taron mutane marasa kula suna kewaye da ita; aka kawo Sabenawa†
daga hamada tare da mutane daga mashaya, suka sa mundaye a hannuwan macen da
kuma ʼyarʼuwarta suka kuma sa rawani masu kyau a kawunansu. 43 Sai na yi magana
a kan wadda ta ƙare ƙarfi ta wurin karuwanci na ce, 'Yanzu bari su yi amfani da ita
kamar karuwa, gama abin da take ke nan.' 44 Suka kuwa kwana da ita. Kamar yadda
maza suke kwana ta karuwa, haka suka kwana da waɗannan lalatattun mata, Ohola
da Oholiba. 45 Amma masu adalci za su hukunta su irin da akan yi wa matan da suka
yi zina suka kuma yi kisa, domin su mazinata ne kuma jini yana a hannuwansu.
46 "Ga abin da Ubangiji Mai Iko Duka yana cewa kawo taron mutane a kansu a
kuma miƙa su don a firgitar da su a kuma washe su. 47 Taron mutanen za su jajjefe
su, su kuma sassare su da takuba; za su kashe ʼyaʼyansu maza da mata su kuma ƙone
gidajensu.
48 "Ta haka zan kawo ƙarshe ga lalaci a ƙasar, don dukan mata su ji gargaɗi
kada kuma su kwaikwaye ku 49 Za ku sha hukuncin lalacinku ku kuma ɗauki hakkin
zunuban bautar gumaka. Saʼan nan za ku san cewa Ni ne Ubangiji Mai Iko Duka."

# 24

*Tukunyar dahuwa*

1 A shekara ta tara, a wata na goma, a rana ta goma, maganar Ubangiji ta zo mini
cewa, 2 "Dan mutum, ka rubuta wannan rana, wannan rana, domin sarkin Babilon
ya yi ƙawanya wa Urushalima a wannan rana. 3 Ka faɗa wa wannan gidan ʼyan
tawaye wani misali ka kuma faɗa musu cewa, 'Ga abin da Ubangiji Mai Iko Duka
yana cewa,
" 'Ka sa tukunyar dahuwa; ka sa ta a kan wuta
ka kuma zuba ruwa a cikinta.

* **23:37** Ko kuwa har sun mai da ʼyaʼyan da suka haifa mini su ratsa cikin wuta † **23:42** Ko kuwa bugaggu

4 Ka sa gunduwoyin nama a cikinta
dukan gunduwoyi masu kyau, cinya da kafaɗa.
Ka cika ta da waɗannan ƙasusuwa mafi kyau;
5 ka kama mafi kyau daga cikin garken.
Ka tara itace a ƙarƙashinta saboda ƙasusuwan;
ka sa ta tafasa
ka kuma dafa ƙasusuwan a cikinta.
6 " 'Gama wannan shi ne abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa,
" 'Kaito birnin nan mai zubar da jini,
ga tukunya wadda take da tsatsa,
wadda tsatsarta ba za tă fita ba!
Ka fitar da shi gunduwa-gunduwa
ba tare da jefa ƙuri'a a kansu ba.

7 " 'Gama zubar da jini yana a tsakiyarta,
ta zubar da shi a dutsen da yake a fili;
ba tă zubar da shi a ƙasa ba,
inda ƙura za tă rufe shi.
8 Don a zuga hasala a kuma yi sakayya
na sa jininta a dutsen da ba a rufe ba,
saboda kada a rufe.
9 " 'Saboda haka ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa,
" 'Kaito birnin nan mai zubar da jini!
Ni ma zan jibge itace da yawa.
10 Ka tula gumagumai
ka kuma ƙuna wuta.
Ka dafa naman da kyau,
kana haɗawa da yaji;
ka kuma bar ƙasusuwan su ƙone.
11 Sa'an nan ka sa tukunyan nan da babu kome a kan garwashi
sai ta yi zafi har darmarta ta yi ja wur
domin dattinta ya narke
tsatsarta kuma ta ƙone.
12 Ta gajiyar da dukan ƙoƙari;
ba a fid da tsatsarta nan mai yawa ba,
kai, ko a wuta ma.
13 " 'Yanzu ƙazantarki ita ce lalaci. Domin na yi ƙoƙari in tsabtacce ke amma ba ki tsabtattu daga ƙazantarki ba, ba za ki ƙara yin tsabta ba sai hasalata a kanki ya kwanta.

14 " 'Ni UBANGIJI na faɗa. Lokaci ya zo da zan aikata. Ba zan janye ba; ba zan ji tausayi ba, ba kuwa zan bari ba. Za a hukunta ki bisa ga hali da ayyukanki, in ji UBANGIJI Mai Iko Duka.' "

### *Matar Ezekiyel ta rasu*

15 Maganar UBANGIJI ta zo mini cewa, 16 "Dan mutum, da farat ɗaya ina gab da
ɗauke abin da idanunka suke jin daɗin gani. Duk da haka kada ka yi makoki ko
ka yi kuka ko ka zub da hawaye. 17 Ka yi nishi shiru; kada ka yi makoki saboda
matacciyar. Ka naɗa rawaninka ka kuma sa takalmanka a ƙafa; kada ka rufe sashen
fuskarka daga ƙasa ko ka ci abincin da masu kuka sukan ci."
18 Da gari ya waye, sai na yi magana da mutane, da yamma kuwa matata ta rasu.
Kashegari na yi yadda aka umarce ni.

19 Sai mutane suka tambaye ni suka ce, “Ba za ka faɗa mana abin da waɗannan
abubuwa suke nufi a gare mu ba?”

20 Sai na ce musu, “Maganar Ubangiji ta zo mini cewa 21 faɗa wa gidan Isra’ila,
‘Ga abin da Ubangiji Mai Iko Duka yana cewa ina gab da ƙazantar da wuri mai
tsarkina, kagarar da kuke taƙama, abin da idanunku suke jin daɗin gani, abin faranta
zuciyarku. ’Ya’yanku maza da mata waɗanda kun bari a baya za su mutu ta wurin
takobi. 22 Za ku kuma yi yadda na yi. Ba za ku rufe sashe ƙasa na fuskarku ko ku ci
abinci da masu kuka sukan ci ba. 23 Za ku naɗa rawunanku a kai ku sa takalmanku
a ƙafafunku. Ba za ku yi kuka ko makoki ba amma za ku lalace saboda zunubanku
ku kuma yi ta yin nishi. 24 Ezekiyel zai zama alama gare ku; za ku yi daidai yadda
ya yi. Sa’ad da wannan ya faru, za ku san cewa ni ne Ubangiji Mai Iko Duka.’

25 “Kai kuma ɗan mutum, a ranar da zan ɗauke musu kagararsu, farin cikinsu da
darajarsu, abin da idanunsu ke jin daɗin gani, abin da yake faranta musu zuciya, da
kuka ’ya’yansu maza da mata, 26 a ranan nan wanda ya tsere zai zo don yǎ ba ka
labari. 27 A lokacin bakinka zai buɗe, za ka yi magana da shi ba kuwa za ka ƙara yin
shiru ba. Ta haka za ka zama alama gare su, za su kuwa san cewa ni ne Ubangiji.”

# 25

### *Annabci a kan Ammon*

1 Maganar Ubangiji ta zo mini cewa, 2 “Dan mutum, ka fuskanci wajen Ammonawa
ka kuma yi annabci a kansu. 3 Ka ce musu, ‘Ku ji maganar Ubangiji Mai Iko Duka.
Ga abin da Ubangiji Mai Iko Duka yana cewa domin kun ce “Yauwa” a kan wuri mai
tsarkina sa’ad da aka ƙazantar da shi da kuma a kan ƙasar Isra’ila sa’ad da aka mai
da ita kufai da lokacin da aka kai mutanen Yahuda bautar talala, 4 saboda haka zan
ba da ku ga mutanen Gabas abin mallaka. Za su kafa sansanoninsu su yi tentunansu
a cikinku; za su ci ’ya’yan itatuwanku su kuma sha madararku. 5 Zan mai da Rabba
wurin kiwo don raƙuma, Ammon kuma wurin hutu don tumaki. Sa’an nan za ku
san cewa ni ne Ubangiji. 6 Gama ga abin da Ubangiji Mai Iko Duka yana cewa domin
kun tafa hannuwanku kuka kuma buga ƙafafunku, kuna farin ciki don nuna dukan
ƙiyayyarku a kan ƙasar Isra’ila, 7 saboda haka zan miƙa hannuna gāba da ku in
kuma ba da ku ganima ga al’ummai. Zan datse ku daga al’ummai in kuma kore ku
daga ƙasashe. Zan hallaka ku, za ku kuwa san cewa ni ne Ubangiji.’ ”

### *Annabci a kan Mowab*

8 “Ga abin da Ubangiji Mai Iko Duka yana cewa, ‘Domin Mowab da Seyir sun ce,
“Duba, gidan Yahuda ta zama sauran al’ummai,” 9 saboda haka zan buɗe ƙofar shiga
Mowab, farawa daga garuruwan da suke kan iyaka, Bet-Yeshimot, Ba’al-Meyon da
Kiriyatayim, darajar ƙasar. 10 Zan ba da Mowabawa tare da Ammonawa ga mutanen
Gabas abin mallaka, don kada a ƙara tuna da Ammonawa a cikin al’ummai; 11 zan
hukunta Mowabawa. Ta haka za su san cewa ni ne Ubangiji.’ ”

### *Annabci a kan Edom*

12 “Ga abin da Ubangiji Mai Iko Duka yana cewa, ‘Domin Edom ya ɗauki wa kanta
fansa a kan gida Yahuda, ta yi babban laifi ta wurin yin haka, 13 saboda haka ga
abin da Ubangiji Mai Iko Duka yana cewa zan miƙa hannuna a kan Edom in kashe
mutanenta da dabbobinsu. Zan sa ta zama kufai, kuma tun daga Teman har zuwa
Dedan za a kashe su da takobi. 14 Zan ɗau fansa a kan Edom ta hannun mutanena
Isra’ila, za su kuwa hukunta Edom bisa ga fushina da hasalata; za su san sakayyata,
in ji Ubangiji Mai Iko Duka.’ ”

### *Annabci a kan Filistiya*

15 “Ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa, ‘Domin Filistiyawa sun yi sakayya,
suka ɗauki fansa da mugunta a zukatansu, da kuma daɗaɗɗen ƙiyayya sun nemi su
hallaka Yahuda, 16 saboda haka ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa ina
gab da miƙa hannuna a kan Filistiyawa, zan kuwa datse Keretawa in kuma hallaka
waɗanda suka rage a bakin teku. 17 Zan yi musu babbar sakayya da hukunci mai
tsanani cikin hasalata. Sa’an nan za su san cewa ni ne UBANGIJI, sa’ad da na ɗauki
fansa a kansu.’ ”

# 26

*Annabci a kan Taya*
1 A shekara ta goma sha ɗaya, a rana ta fari ga wata, maganar UBANGIJI ta zo mini
cewa, 2 “Ɗan mutum, domin Taya ta yi magana a kan Urushalima ta ce, ‘Yauwa!
Kofar zuwa al’ummai ta karye, an kuma buɗe mini ƙofofinta; yanzu da take kufai
zan wadace,’ 3 saboda haka ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa ina gāba
da ke, ya Taya, zan kuwa kawo al’ummai masu yawa su yi gāba da ke, kamar yadda
teku takan kawo raƙuman ruwa. 4 Za su hallaka katangar Taya su kuma rurrushe
hasumiyoyinta; zan kankare tarkacenta, in maishe ta fā. 5 Za tă zama wurin shanya
abin kamun kifi a tsakiyar teku, gama na faɗa, in ji UBANGIJI Mai Iko Duka. Za tă
zama ganima ga sauran al’ummai, 6 za a kashe mazaunan filin ƙasar da takobi. Ta
haka za su san cewa ni ne UBANGIJI.
7 “Gama ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa daga arewa zan kawo wa
Taya Nebukadnezzar* sarkin Babilon, sarkin sarakuna, tare da dawakai da kekunan
yaƙi, da mahayan dawakai da babbar rundunar soja. 8 Zai kashe mazaunan filin
ƙasar da takobi; zai yi miki ƙawanya, ya gina miki mahaurai, sa’an nan ya rufe ki
da garkuwoyi. 9 Zai rushe katangarki da dundurusai, ya rurrushe hasumiyoyinki da
makamai. 10 Dawakansa za su yi yawa har su rufe ke da ƙura. Katanga za su girgiza
saboda motsin dawakan yaƙi, kekunan doki da keken yaƙin sa’ad da suka shiga birnin
da aka rushe katangar. 11 Kofatan dawakansa za su tattake dukan titunanki; zai
kashe mutanenki da takobi, ginshiƙanki masu ƙarfi kuma za su fāɗi a ƙasa. 12 Za su
washe dukiyarki, kayan cinikinki kuma su zama ganima; za su rurrushe katangarki
su ragargaza gidajenki masu kyau su kuma zubar da duwatsunki, katakanki da kuma
tarkacenki a cikin teku. 13 Zan kawo ƙarshen waƙoƙinki masu surutu, ba kuwa za
a ƙara jin kaɗe-kaɗen garayunki ba. 14 Zan maishe ki fā, za ki kuma zama wurin
shanya abin kamun kifi. Ba za a sāke gina ki ba, gama Ni UBANGIJI na faɗa, in ji
UBANGIJI Mai Iko Duka.
15 “Ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa wa Taya. Kasashen da suke a
bakin teku ba za su girgiza saboda ƙarar fāɗuwarki, sa’ad da nishin waɗanda aka yi
wa rauni da kashe-kashen da aka yi a cikinki suka faru ba? 16 Sa’an nan sarakunan
bakin teku za su sauka daga gadajen sarautarsu, su tuɓe rigunansu, da rigunansu
waɗanda aka yi wa ado. Za su zauna a ƙasa suna rawar jiki a kowane lokaci suna
razana saboda abin da ya same ki. 17 Sa’an nan za su yi makoki game da ke su ce,

“ ‘Yaya kika hallaka haka nan, ya birnin da ta yi suna,
cike da mutanen teku!
Ke da kika zama mai ƙarfi cikin tekuna,
ke da mazauna cikinki;
kin sa tsoronki
a kan dukan waɗanda suka zauna a can.
18 Yanzu tsibirai suna rawar jiki

* **26:7** Da Ibraniyanci Nebukadrezzar, wanda Nebukadnezzar wata hanyar ce na rubuta sunan; a nan da kuma sau da yawa Ezekiyel da Irmiya sun cika amfani da wannan hanyar rubuta sunan.

a ranar fāɗuwarki;
tsibirai a cikin teku
sun tsorata a ɓacewarki.'
19 "Ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa sa'ad da na maishe ki kufai, kamar
sauran biranen da ba a ƙara zama a ciki, sa'ad da kuma na kawo zurfafan teku a
kanki da yawan ruwansa suka rufe ki, 20 a sa'an nan zan sauko da ke ƙasa tare da
waɗanda suke gangarawa zuwa rami, zuwa wurin mutanen dā. Zan sa ki zauna
ƙarƙashin ƙasa, kamar a kufai na tun dā, tare da waɗanda suke gangarawa zuwa
rami, ba kuwa za ki ƙara dawowa ba ko ki ɗauki matsayinki† a ƙasar masu rai. 21 Zan
sa ki yi mummunan ƙarshe kuma ba za ki ƙara kasancewa ba. Za a neme ki, amma
ba za a ƙara same ki ba, in ji UBANGIJI Mai Iko Duka."

# 27

*Makoki domin Taya*

1 Maganar UBANGIJI ta zo mini cewa, 2 "Dan mutum, ka yi makoki domin Taya.
3 Ka ce wa Taya, wadda take zaune a hanyar shiga zuwa teku, kasuwar masu yawa
mutane a bakin teku, 'Ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa,
" 'Kin ce, ya Taya,
"Ni kyakkyawa ce cikakkiya."
4 Manyan tekuna ne wurin zamanki;
maginanki sun sa kyanki ya zama cikakke.
5 Sun yi dukan katakanki
daga itatuwan fir daga Senir;*
sun kwaso itatuwan al'ul daga Lebanon
don su yi miki jigon jirgin ruwa.
6 Da oak daga Bashan
suka yi sandunan tuƙan jirgin ruwa
da itatuwan kasharina daga bakin tekun Saifurus
suka yi daɓe jirgin ruwanki, suka kuma manne masa hauren giwa.
7 Lilin mai kyau mai ado daga Masar ne filafilan jirgin ruwanki
suka kuma zama tutarki;
an yi tutarki da shuɗi da shunayya
daga bakin tekun Elisha.
8 Mutanen Sidon da Arfad su ne matuƙan jirgin ruwanki;
gwanayenki, ya Taya, suna ciki a matsayi matuƙan jiragen ruwa.
9 Masu hikima na Gebal† suna ciki
a matsayin masu tattoshe mahaɗan katakon jirginki.
Dukan jiragen ruwa da matuƙansu
sukan zo wurinki don kasuwanci.

10 " 'Mutanen Farisa, Lidiya da Fut
su ne suka zama sojoji a cikin mayaƙanki.
Sun rataye garkuwoyinsu da hulunan kwano a katangarki,
suna kawo miki daraja.
11 Mutanen Arfad da Helek
sun yi tsaron katangar a kowace gefe;
mutanen Gammad
su ne a hasumiyoyinki.
Sun rataye garkuwoyinsu kewaye da katangarki;

† **26:20** Seftuwajin; Da Ibraniyanci dawo, zan kuma ba da darajarki * **27:5** Wato, Hermon † **27:9** Wato, Baibilos

sun sa kyanki ya zama cikakke.
12 " 'Tarshish ta yi ciniki da ke saboda yawan wadatar kayayyakinki; sun sayi kayan
cinikinki da azurfa, ƙarfe, kuza da dalma.
13 " 'Girka, Tubal da Meshek sun yi kasuwanci da ke; sun sayi kayanki suka biya da
bayi da kuma abubuwan da aka yi da tagulla.
14 " 'Mutanen Bet Togarma sun sayi kayan cinikinki da dawakai, dawakan yaƙi da
alfadarai.
15 " 'Mutanen Dedan sun yi kasuwanci da ke, bakin teku masu yawa abokan
cinikinki ne; sun biya ki da hauren giwa da katakon kanya.
16 " 'Mutanen Aram‡ sun yi ciniki da ke saboda yawan kayanki; suka sayi kayan
cinikinki da zumurrudu, da shunayya, da kayan ado, da lilin mai taushi, da murjani,
da yakutu.
17 " 'Yahuda da Isra'ila sun yi kasuwanci da ke; sun sayi kayanki da alkama da
Minnit da alawa,§ da zuma, da mai, da ganyaye masu ƙanshi.
18 " 'Mutanen Damaskus sun ga abin da za ki iya bayarwa sai suka yi ciniki da ke,
ta sayi kayanki da ruwan inabi daga Helbon, da ulu daga Zahar. 19 Wedan da Yaban
kusa da Uzal, suka sayi kayanki; wato gyararren ƙarfe da kayan yaji.
20 " 'Mutanen Dedan sun sayi kayanki da sirdin zama a kan dawakai.
21 " 'Mutanen Arabiya da dukan sarakunan Kedar abokan cinikinki ne; sun yi ciniki
da ke suka sayi kayanki da 'yan raguna, da raguna, da awaki.
22 " ''Yan kasuwan Sheba da Ra'ama sun yi ciniki da ke; suka sayi kayanki da kayan
yaji mafi kyau iri-iri, da duwatsu masu daraja iri-iri, da zinariya.
23 " 'Haran, Kanne da Eden da kuma 'yan kasuwan Sheba, Assuriya da Kilmad sun
yi ciniki da ke. 24 A kasuwarki sun yi ciniki da ke suka sayar miki tufafi masu tsada, da
na shuɗi, da masu ado, da dardumai masu ƙyalƙyali da kirtani, da igiyoyi waɗanda
aka tuƙa da kyau.

25 " 'Jiragen ruwan Tarshish sun zama
masu jigilar kayanki.
Kin cika da kaya masu nauyi
a tsakiyar teku.
26 Matuƙan jiragenki sun kai ki
can cikin manyan tekuna.
Amma iskar gabas za tă farfasa ki kucu-kucu
a tsakiyar teku.
27 Dukiyarki, cinikinki da kayan kasuwarki,
ma'aikatanki na jirgi, matuƙan jiragenki da masu tattoshe mahaɗan katakan jiragenki,
'yan kasuwarki da dukan sojojinki,
da kuma kowa da yake cikin jirgi
zai nutsa a tsakiyar teku
a ranar da jirginki zai nutse.
28 Kasashen bakin teku za su girgiza
sa'ad da matuƙan jirginki suka yi kuka.
29 Dukan waɗanda suke riƙe da matuƙi
za su ƙyale jiragensu;
ma'aikatan jirage da dukan matuƙan jirage
za su tsaya a bakin teku.
30 Za su tā da muryarsu

‡ **27:16** Da yawa cikin rubuce-rubucen hannu na Ibraniyanci; waɗansu rubuce-rubucen hannu na Ibraniyanci da na Siriyak Edom § **27:17** Ma'anar Ibraniyanci na wannan kalma babu tabbas.

su yi kuka mai zafi a kanki;
za su yayyafa ƙura a kawunansu,
su yi ta birgima a cikin toka.
31 Za su aske kawunansu saboda ke
za su kuma sa tufafin makoki.
Za su yi kuka dominki su yi ɓacin rai
da kuma kuka mai zafi.
32 Yayinda suke kuka a kanki kuwa,
za su yi makoki dominki suna cewa,
"Wa ya taɓa yin shiru kamar Taya,
kewaye da teku?"
33 Sa'ad da kayan cinikinki suka tafi ƙasashen hayi,
kin gamsar da al'ummai masu yawa;
da dukiyarki masu yawa da kuma kayan cinikinki
kin azurtar da sarakunan duniya.
34 Yanzu teku ta farfashe ki
cikin zurfafan ruwaye;
kayan cinikinki da dukan kamfaninki
sun nutse tare da ke.
35 Dukan mazaunan bakin teku
sun giggice saboda masifarki;
sarakunansu sun tsorata ƙwarai
fuskokinsu kuwa sun yamutse don tsoro.
36 'Yan kasuwa a cikin al'ummai suna yin miki tsaki;
kin zo ga mummunar ƙarshe
ba za ki ƙara kasancewa ba har abada.' "

# 28

*Annabci a kan sarkin Taya*

1 Maganar UBANGIJI ta zo mini cewa, 2 "Dan mutum, ka faɗa wa mai mulkin Taya
cewa, 'Ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa,
" 'Cikin alfarmar zuciyarka
ka ce, "Ni allah ne;
ina zama a kan kursiyin allah
a tsakiyar tekuna."
Amma kai mutum ne ba allah ba,
ko da yake ka ɗauka kana da hikima kamar allah.
3 Ka fi Daniyel hikima ne?*
Ba asirin da yake ɓoye a gare ka?
4 Ta wurin hikimarka da ganewarka
ka sami dukiya wa kanka
ka kuma tara zinariya da azurfa
cikin wuraren ajiyarka.
5 Ta wurin dabararka mai girma cikin kasuwanci
ka ƙara dukiyarka,
kuma saboda dukiyarka
zuciyarka ta cika da alfarma.
6 " 'Saboda haka ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa,
" 'Domin ka ɗauka kai mai hikima ne,

* **28:3** Ko kuwa Danel; yadda aka rubuta Ibraniyanci na wannan suna zai yi kamar ana zance wani dabam ne da annabi Daniyel.

mai hikima kamar allah,
[7] zan kawo baƙi a kanka,
waɗanda suka fi mugunta cikin sauran al'ummai;
za su zāre takubansu a kan kyakkyawar hikimarka
su kuma ɓarke darajarka mai walƙiya.
[8] Za su jefar da kai cikin rami,
za ka kuwa yi muguwar mutuwa
a tsakiyar tekuna.
[9] Za ka iya ce yanzu, "Ni allah ne,"
a gaban waɗanda suka kashe ka?
Za ka zama mutum kurum, ba allah ba,
a hannuwan waɗanda suka kashe ka.
[10] Za ka yi mutuwar marar kaciya
a hannuwan baƙi.
Na faɗa, in ji UBANGIJI Mai Iko Duka.' "

[11] Maganar UBANGIJI ta zo mini cewa, [12] "Ɗan mutum, ka yi makoki domin sarkin
Taya ka kuma ce masa, 'Ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa,
" 'Ka kasance hatimin cikakke,
cike da hikima da cikakke a kyau.
[13] Ka kasance a Eden,
a lambun Allah;
aka yi maka ado da kowane dutse mai daraja,
yakutu, tofaz, da zumurrudu,
kirisolit, onis da yasfa,
saffaya,† turkuwoyis da beril.
Tsare-tsare da shirye-shiryenka an yi su da zinariya ne;
a ranar da aka halicce ka an shirya su.
[14] An shafe ka kamar kerub mai tsaro,
gama haka na naɗa ka.
Kana a tsattsarkan dutsen Allah;
ka yi tafiya a tsakiyar duwatsun wuta.
[15] Ka kasance marar laifi cikin dukan hanyoyinka
daga ranar da aka halicce ka
sai da aka sami mugunta a cikinka.
[16] Ta wurin yawan kasuwancinka
ka cika da rikici,
ka kuma yi zunubi.
Saboda haka na kore ka da kunya daga dutsen Allah,
na kore ka, ya kerub mai tsaro,
daga cikin duwatsun wuta.
[17] Zuciyarka ta cika da alfarma
saboda kyanka,
ka kuma lalace hikimarka
saboda darajarka.
Saboda haka na jefar da kai zuwa ƙasa;
na sa ka zama abin kallo a gaban sarakuna.
[18] Ta wurin yawan zunubanka da kasuwancinka na cuta
ka ƙazantar da wuri mai tsarkinka.
Saboda haka na sa wuta ta fito daga cikinka,
ta cinye ka,

---
† **28:13** Ko kuwa lafis lazuli

na maishe ka toka a bisa ƙasa
a kan idon dukan waɗanda suke kallonka.
19 Dukan al'umman da suka san ka
sun giggice saboda masifar da ta auko maka;
ka zo ga mummunar ƙarshe
ba za ka ƙara kasancewa ba har abada.' "

### *Annabci a kan Sidon*

20 Maganar UBANGIJI ta zo mini cewa, 21 "Dan mutum, ka fuskanci Sidon; ka yi
annabci a kanta 22 ka ce, 'Ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa,
" 'Ina gāba da ke, ya Sidon,
zan sami ɗaukaka a cikinki.
Za su san cewa ni ne UBANGIJI,
sa'ad da na zartar da hukunci a kanta
na kuma nuna kaina mai tsarki a cikinta.
23 Zan aika da annoba a kanta
in kuma sa jini ya zuba a titunanta.
Kisassu za su fāɗi a cikinta,
da takobi yana gāba da ita a kowane gefe.
Sa'an nan za su san cewa ni ne UBANGIJI.
24 " 'Mutanen Isra'ila ba za su ƙara kasance da mugayen maƙwabta waɗanda za
su zama sarƙaƙƙiya masu zafi da ƙaya mai tsini ba. Sa'an nan za su san cewa ni ne
UBANGIJI Mai Iko Duka.
25 " 'Ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa sa'ad da na tattara mutanen
Isra'ila daga al'ummai inda suke a warwatse, zan nuna kaina mai tsarki a cikinsu a
idon al'ummai. Sa'an nan za su zauna a ƙasarsu, wadda na ba wa bawana Yaƙub.
26 Za su zauna a can lafiya su kuma gina gidaje su nome gonakin inabi; za su zauna
lafiya sa'ad da zan zartar da hukunci a kan dukan maƙwabtansu da suka wulaƙanta
su. Sa'an nan za su san cewa ni ne UBANGIJI Allahnsu.' "

## 29

### *Annabci a kan Masar*

1 A shekara ta goma, a wata na goma, a rana ta goma sha biyu, maganar UBANGIJI ta
zo mini cewa, 2 "Dan mutum, ka fuskanci Fir'auna sarkin Masar ka kuma yi annabci
gāba da shi da dukan Masar. 3 Yi masa magana ka ce, 'Ga abin da UBANGIJI Mai Iko
Duka yana cewa,
" 'Ina gāba da kai, Fir'auna sarkin Masar,
kai babban mugun dodon ruwa kwance cikin rafuffukanka.
Ka ce, "Nilu nawa ne;
na yi shi wa kaina."
4 Amma zan sa ƙugiyoyi a muƙamuƙanka
in sa kifin rafuffukanka su manne wa kamɓorinka.
Zan jawo ka daga cikin tsakiyar rafuffukanka,
da dukan kifayen rafuffukanka, waɗanda suka manne a ƙamborinka,
5 Zan bar ka a cikin hamada,
kai da dukan kifin rafuffukanka.
Za ka fāɗi a fili
ba kuwa za a tattara ka ko a kwashe ba.
Zan ba da kai kamar abinci
ga namun jeji na duniya da tsuntsayen sararin sama.
6 Ta haka dukan waɗanda suke zama a Masar za su san cewa ni ne UBANGIJI.

“ ‘Ka zama sandan iwa domin gidan Isra’ila. 7 Sa’ad da suka kama ka da
hannuwansu, ka tsattsage, ka kuma buɗu a kafaɗunsu; sa’ad da suka jingina a kanka,
sai ka karye, bayansu kuwa ya firgita.[*]
8 “ ‘Saboda haka ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa zan kawo takobi a
kanka in kashe mutane da dabbobi. 9 Masar za tă zama kufai. Sa’an nan za su san
cewa ni ne UBANGIJI.
“ ‘Domin ka ce, “Nilu nawa ne; ni na yi shi,” 10 saboda haka ina gāba da kai da
rafuffukanka, zan kuma maishe ƙasar Masar ta lalace ta kuma zama kango daga
Migdol zuwa Aswan, har iyakar Kush.[†] 11 Ba ƙafar mutum ko ta dabbar da za tă ratsa
ta; ba wanda zai zauna a can har shekaru arba’in. 12 Zan mai da ƙasar Masar kufai
a cikin ƙasashen da aka ragargaza, biranenta kuma za su zama kango har shekaru
arba’in a cikin biranen da aka lalace. Zan watsar da Masarawa a cikin al’ummai in
warwatsa su cikin ƙasashe.
13 “ ‘Duk da haka ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa a ƙarshen shekaru
arba’in ɗin zan tattara Masarawa daga al’ummai inda aka warwatsa su. 14 Zan komo
da su daga zaman bauta in mai da su zuwa Masar ta Bisa,[‡] ƙasarsu ta ainihi. A
can za su zama masarauta marar ƙarfi. 15 Za tă zama masarauta mafi rarrauna cikin
masarautai, ba kuwa za tă ƙara ɗaga kanta a kan sauran al’ummai ba. Zan sa tă zama
marar ƙarfi ƙwarai, har da ba za tă ƙara yin mulkin a kan al’ummai ba. 16 Masar
ba za tă ƙara zama abin dogara ga mutanen Isra’ila ba amma za tă zama abin tunin
zunubinsu na juyawa gare ta don taimako. Sa’an nan za su san cewa ni ne UBANGIJI
Mai Iko Duka.’ ”
17 A shekara ta ashirin da bakwai, a wata na fari a rana ta farko, maganar UBANGIJI
ta zo mini cewa, 18 “Ɗan mutum, Nebukadnezzar sarkin Babilon ya sa sojojinsa su
matsa wa Taya; kowane kai ya koɗe, kowace kafaɗa kuma ta goge. Duk da haka shi
da sojojinsa ba su sami wani lada daga matsin da suka yi a kan Taya ba. 19 Saboda
haka ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa zan ba da Masar ga Nebukadnezzar
sarkin Babilon, zai washe dukiyarta. Zai kwashe ya washe ƙasar ganima a matsayin
abin biyan sojojinsa. 20 Saboda haka na ba shi Masar a matsayin lada don ƙoƙarinsa
domin shi da sojojinsa sun yi wannan domina ne, in ji UBANGIJI Mai Iko Duka.
21 “A wannan rana zan sa ƙaho[§] ya tsiro wa gidan Isra’ila, zan kuma buɗe bakinka
a cikinsu. Sa’an nan za su san cewa ni ne UBANGIJI.”

# 30

### *Makoki domin Masar*

1 Maganar UBANGIJI ta zo mini cewa, 2 “Ɗan mutum, ka yi annabci ka ce, ‘Ga abin
da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa,
“ ‘Yi kuka kana cewa,
“Kaito saboda wannan rana!”
3 Gama ranar ta yi kusa,
ranar UBANGIJI ta gabato,
ranar gizagizai,
lokacin hallaka wa al’ummai.
4 Takobi zai zo a kan Masar,
azaba za tă zo a kan Kush.
Sa’ad da kisassu za su fāɗi a Masar,
za a kwashe dukiyarta a tafi
a rushe harsashinta.
5 Kush da Fut, Lidiya da dukan Arabiya, Libiya[*] da kuma mutanen ƙasar alkawari

[*] **29:7** Siriyak (dubi kuma Seftuwajin da Bulget); Da Ibraniyanci ka kuma sa bayansu suka tsaya [†] **29:10** Wato, yankin bisa Nilu [‡] **29:14** Da Ibraniyanci zuwa Faturos [§] **29:21** Kaho a nan yana nuna alamar ƙarfi ne. [*] **30:5** Da Ibraniyanci Kub

za su mutu ta wurin takobi tare da Masar.
6 " 'Ga abin da UBANGIJI ya faɗa,
" 'Waɗanda suke goyon bayan Masar za su fāɗi
ƙarfinta da take fariya da shi zai ƙare.
Daga Migdol zuwa Aswan
za su mutu ta wurin takobi a cikinta,
in ji UBANGIJI Mai Iko Duka.
7 Za su zama kango
a cikin ƙasashen da suke kango,
biranensu kuwa za su zama kufai
a cikin biranen da suka lalace.
8 Sa'an nan za su san cewa ni ne UBANGIJI,
sa'ad da suka ga na sa wuta wa Masar
aka kuma ragargaza masu taimakonta.
9 " 'A wannan rana manzanni za su fito daga wurina a jiragen ruwa don su tsorata
Kush daga sake jikinta. Azaba za tă kama su a ranar hallakar Masar, gama tabbatacce
za tă zo.

10 " 'Ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa,
" 'Zan kawo ƙarshen mutanen Masar
ta hannun Nebukadnezzar sarkin Babilon.
11 Shi da sojojinsa, mafi bantsoro cikin al'ummai,
za a kawo don su hallaka ƙasar.
Za su zāre takuba a kan Masar
su kuma cika ƙasar da kisassu.
12 Zan kafe rafuffukan Nilu
in sayar da ƙasar ga mugayen mutane;
ta hannun baƙi
zan sa ƙasar ta lalace da kome da yake cikinta.
Ni UBANGIJI na faɗa.

13 " 'Ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa,
" 'Zan hallaka gumaka
in kuma kawo ƙarshen siffofi a Memfis.†
Ba za a ƙara samun yerima a ƙasar Masar ba,
zan kuma baza tsoro a duk fāɗin ƙasar.
14 Zan lalace Masar ta Bisa‡
in ƙuna wuta wa Zowan
in zartar da hukunci a kan Tebes.§
15 Zan kwarara hasalata a kan Felusiyum,*
kagarar Masar,
in kuma datse mutanen Tebes.
16 Zan ƙuna wuta wa Masar;
Felusiyum za tă sha azaba mai zafi.
Za a tayar wa Tebes da hankali;
Memfis za tă riƙa kasance cikin ɓacin rai.
17 Samarin Heliyofolis† da Bubastis‡
za su mutu ta wurin takobi,
biranen kansu za su tafi bauta.
18 Duhu ne zai zama rana a Tafanes
sa'ad da na karye ikon Masar;

---

† **30:13** Da Ibraniyanci Nof; haka ma a aya 16. ‡ **30:14** Da Ibraniyanci lalace Faturos § **30:14** Da Ibraniyanci No; haka ma a ayoyi 15 da 16. * **30:15** Da Ibraniyanci Sin; haka ma a ayar 16. † **30:17** Da Ibraniyanci Awen (ko On). ‡ **30:17** Da Ibraniyanci Fi Beset

a can ƙarfin da take fariya zai ƙare.
Za a rufe ta da gizagizai
ƙauyukanta kuma za su tafi bauta.
19 Ta haka zan zartar da hukunci a kan Masar,
za su kuwa san cewa ni ne UBANGIJI.' "

### *An Karye Hannuwan Fir'auna*

20 A shekara ta goma sha ɗaya, a wata na fari a rana ta goma sha bakwai, maganar
UBANGIJI ta zo mini cewa, 21 "Ɗan mutum, na karye hannun Fir'auna sarkin Masar.
Ba a ɗaure shi don warkarwa ba ko a sa tsinke saboda kada yă zama da ƙarfi har
ya riƙe takobi. 22 Saboda haka ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa ina
gāba da Fir'auna sarkin Masar. Zan karye hannuwansa biyu, hannun da yake da
kyau da kuma wanda an riga an karya, in kuma sa takobi ya fāɗi daga hannunsa.
23 Zan watsar da Masarawa a cikin al'ummai in warwatsa su cikin ƙasashe. 24 Zan
ƙarfafa hannuwan sarkin Babilon in kuma sa takobina a hannunsa, amma zan karya
hannuwan Fir'auna, zai kuwa yi nishi a gabansa kamar mutumin da aka yi wa raunin
mutuwa. 25 Zan ƙarfafa hannuwan sarkin Babilon, amma hannuwan Fir'auna za su
shanye. Sa'an nan za su san cewa ni ne UBANGIJI, sa'ad da na sa takobi a hannun
sarkin Babilon na kuma miƙa shi a kan Masar. 26 Zan watsar da Masarawa a cikin
al'ummai in warwatsa su cikin ƙasashe. Sa'an nan za su san cewa ni ne UBANGIJI."

# 31

### *Al'ul a Lebanon*

1 A shekara ta goma sha ɗaya, a wata na uku a rana ta farko, maganar UBANGIJI ta
zo mini cewa, 2 "Ɗan mutum, faɗa wa Fir'auna sarkin Masar da jama'arsa cewa,
" 'Da wa za a kwatanta girmanka?
3 Ka dubi Assuriya, ta taɓa zama kamar al'ul a Lebanon
da rassa masu kyau suna inuwartar da kurmi;
ya yi tsayi ainun
kansa ya kai cikin gizagizai.
4 Ruwa ya sa ya yi girma,
zurfafan maɓulɓulai sun sa ya yi tsayi;
rafuffuka suna gudu
kewaye da tushensa
yana aika da rafuffukansa
zuwa dukan itatuwan kurmi.
5 Saboda haka ya yi tsayi
fiye da sauran itatuwan kurmi;
rassansa suka ƙaru
suka yi tsayi,
suka bazu saboda yalwar ruwaye.
6 Dukan tsuntsayen sararin sama
suka yi sheƙa a rassansa,
dukan namun jeji
suka haihu a ƙarƙashin rassansa;
dukan al'ummai
suka zauna a inuwarsa.
7 Yana da girma a kyau,
da dogayen rassansa da ya baza,
gama saiwoyinsa sun nutse can ƙasa
har cikin yalwar ruwaye.
8 Al'ul a cikin lambun Allah

ba su kai shi ba,
balle itatuwan kasharina
su kai rassansa,
ko itatuwan durumi
su kai rassansa,
ko itace a lambun Allah
ya kai kyansa.
9 Na sa ya yi kyau
da yalwar rassa,
abin ƙyashi na dukan itatuwan Eden
a lambun Allah.
10 " 'Saboda haka ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa domin ya yi tsayi,
kansa kuma ya kai cikin gizagizai, kuma domin ya yi fariya saboda tsayinsa, 11 na
miƙa shi ga mai mulkin al'ummai, don yă sāka masa gwargwadon muguntarsa. Na
jefar da shi a gefe, 12 kuma baƙi mafi mugunta na al'ummai suka sare shi suka bar shi.
Rassansa sun fāɗi a kan duwatsun da suke cikin dukan kwaruruka; rassansa kuma
sun kakkarye, sun fāɗi a cikin dukan magudanan ruwa na ƙasa. Dukan al'umman
duniya suka fito daga ƙarƙashin inuwarsa suka bar shi. 13 Dukan tsuntsaye sararin
sama suka zauna a itacen da ya fāɗi, dukan namun jeji kuma suna cikin rassansa.
14 Saboda haka ba wani daga cikin itatuwan da suke kusa da ruwan da zai taɓa yin
fariyar tsawonsa, har kawunansu su kai cikin gizagizai. Ba wani daga cikin itatuwan
da ya sha ruwa sosai da zai taɓa yi wannan tsayi; duk an bashe su ga mutuwa, zuwa
can ƙasa, a cikin matattu, tare da waɗanda suka gangara zuwa rami.
15 " 'Ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa a ranar da aka yi ƙasa da shi
zuwa kabari* na rufe zurfafa maɓulɓulai da makoki dominsa; na janye rafuffukansa,
aka kuma hana yalwan ruwansa. Saboda shi na rufe Lebanon da baƙin ciki, dukan
itatuwan kurmi suka bushe. 16 Na sa al'ummai suka yi rawar jiki da jin ƙarar
fāɗuwarsa sa'ad da na yi ƙasa da shi zuwa kabari tare da waɗanda suka gangara
rami. Sai dukan itatuwan Eden, zaɓaɓɓu da kuma mafi kyau na Lebanon, dukan
itatuwan da aka yi musu banruwa, sun ta'azantu a ƙarƙashin ƙasa. 17 Waɗanda
suka zauna a inuwarsa, dukan masu tarayyarsa a cikin al'ummai, su ma sun gangara
zuwa kabari tare da shi, sun haɗu da waɗanda aka kashe da takobi.
18 " 'Da wa cikin itatuwan Eden za a kwatanta da kai cikin girma da daraja? Duk
da haka kai ma, za a yi ƙasa da kai tare da itatuwan Eden zuwa ƙarƙashin ƙasa; za
ka kwanta a cikin marasa kaciya, tare da waɗanda aka kashe da takobi.
" 'Fir'auna ke nan da dukan jama'arsa, in ji UBANGIJI Mai Iko Duka.' "

# 32

*Makoki domin Fir'auna*

1 A shekara ta goma sha biyu, a wata na goma sha biyu a rana ta fari, maganar
UBANGIJI ta zo mini cewa, 2 "Dan mutum, ka yi makoki a kan Fir'auna sarkin Masar
ka faɗa masa.
" 'Kai kamar zaki ne a cikin al'ummai;
kai kamar dodon ruwa a cikin tekuna
kana ɓullowa cikin rafuffukanka,
kana gurɓata ruwa da ƙafafunka kana kuma dama rafuffuka.
3 " 'Ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa,
" 'Da taron jama'a masu yawa zan jefa abin kamun kifi a kanka,
za su kuwa jawo ka da abin kamun kifi.
4 Zan jefar da kai a ƙasa zan jefa ka a fili.

* **31:15** Da Ibraniyanci Sheol; haka ma yake a ayoyi 16 da 17.

Zan sa dukan tsuntsayen sararin sama su zauna a kanka
dukan namun jeji na duniya kuma za su ƙosar da kansu a kanka.
5 Zan baza namanka a kan duwatsu
in kuma cika kwaruruka da gawarka.
6 Zan jiƙa ƙasar da jininka mai gudu har zuwa duwatsu,
magudanan ruwa za su cika da namanka.
7 Sa'ad da na shafe ka, zan rufe sammai in duhunta taurarinsu;
zan rufe rana da girgije, wata kuwa ba zai ba da haskensa ba.
8 Dukan haskokin sammai za su zama duhu a kanka;
zan kawo duhu a kan ƙasarka,
in ji UBANGIJI Mai Iko Duka.
9 Zan dami zukatan mutane masu yawa
sa'ad da na kawo maka hallaka a cikin al'ummai, a cikin* ƙasashen da ba ka taɓa sani ba.
10 Zan sa mutane da yawa su giggice saboda abin da ya same ka,
sarakunansu kuma za su yi rawar jiki saboda kai sa'ad da na kaɗa takobina a gabansu.
A ranar fāɗuwarka
kowannensu zai yi rawar jiki a kowane lokaci saboda ransa.
11 " 'Gama ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa,
" 'Takobin sarkin Babilon
zai auko maka.
12 Zan sa jama'arka su mutu ta wurin takuban ƙarfafan mutane,
masu bantsoro na dukan al'ummai.
Za su lalatar da girman kan Masar,
su kuma tumɓuke dukan jama'arta.
13 Zan hallaka dukan dabbobinta
da suke kusa da ruwaye masu yawa
ƙafar mutum ba zai ƙara damunsa
ko kofaton dabba ya gurɓata shi.
14 Sa'an nan zan sa ruwanta su kwanta
in sa rafuffukanta su gudu kamar mai,
in ji UBANGIJI Mai Iko Duka.
15 Sa'ad da na mai da Masar kufai
na kuma raba ƙasar da abin da take cike da shi,
sa'ad da na bugi dukan waɗanda suke cikinta,
a sa'an nan ne za su san cewa ni ne UBANGIJI.'
16 "Wannan ne makokin da za a yi mata. 'Yan matan al'ummai za su rera shi; gama
Masar da dukan jama'arta za su rera shi, in ji UBANGIJI Mai Iko Duka."

### *Masar ta Gangara zuwa Cikin Lahira*

17 A shekara ta goma sha biyu, a rana ta goma sha biyar ga wata, maganar UBANGIJI
ta zo mini cewa, 18 "Dan mutum, yi kuka saboda jama'ar Masar ka kuma tura ta da
'yan matan manyan al'ummai zuwa ƙarƙashin ƙasa, tare da waɗanda suka gangara
zuwa rami. 19 Ka ce, 'Kin fi sauran tagomashi ne? Ki gangara, ki kwanta cikin marasa
kaciya.' 20 Za su fāɗi cikin waɗanda aka kashe da takobi. Takobin da an zāre; bari
a ja ta a tafi tare da dukan jama'arta. 21 Daga cikin kabari† manyan shugabanni za
su yi maganar Masar da abokanta su ce, 'Sun gangara sun kuma kwanta da marasa
kaciya, tare da waɗanda aka kashe da takobi.'
22 "Assuriya tana can tare da dukan sojojinta; an kewaye ta da kaburburan dukan
waɗanda aka kashe, dukan waɗanda suka mutu ta wurin takobi. 23 Kaburburansu

* **32:9** Da Ibraniyanci; Seftuwajin kai ka cikin zaman bauta a cikin al'ummai, zuwa

† **32:21** Da Ibraniyanci Sheol; haka ma a aya 27.

suna cikin zurfafan rami kuma sojojinta suna kwance kewaye da kabarinta. Dukan
waɗanda suka haddasa tsoro a ƙasar masu rai sun mutu, an kashe su da takobi.
24 “Elam tana can, tare da dukan jama’arta kewaye da kabarinta. Dukansu sun
mutu, an kashe su da takobi. Dukan waɗanda suka haddasa tsoro a ƙasar masu
rai sun gangara wurin marasa kaciya a duniyar da take ƙarƙashi. Suna shan kunya
tare da waɗanda suka gangara zuwa rami. 25 An yi mata gado a cikin matattu, tare
da dukan jama’arta kewaye da kabarinta. Dukansu marasa kaciya ne, da aka kashe
da takobi. Domin tsoronsu ya bazu cikin ƙasar masu rai, suna shan kunya tare da
waɗanda suka gangara zuwa rami; an kwantar da su tare da waɗanda aka kashe.
26 “Meshek da Tubal suna can, tare da dukan jama’arsu kewaye da kaburburansu.
Dukansu marasa kaciya ne, da aka kashe da takobi domin sun haddasa tsoronsu
a ƙasar masu rai. 27 Ba sun kwanta tare da sauran jarumawa marasa kaciyan
da aka kashe, waɗanda suka gangara kabari tare da makaman yaƙinsu, waɗanda
aka yi musu matashin kai da takubansu ba? Hukuncin zunubansu yana a bisa
ƙasusuwansu, ko da yake tsoron waɗannan jarumawa ya manne cikin ƙasar masu
rai.
28 “Kai kuma, ya Fir’auna, za a kakkarye ka za ka kuma kwanta a cikin marasa
kaciya, tare da waɗanda aka kashe da takobi.
29 “Edom tana can, sarakunanta da dukan yerimanta; duk da ikonsu, sun kwanta
tare da waɗanda aka kashe da takobi. Suna kwance tare da marasa kaciya, tare da
waɗanda suka gangara zuwa rami.
30 “Dukan yerima arewa da dukan Sidoniyawa suna can; sun gangara tare da
waɗanda aka kashe cikin kunya duk da tsoron da suka haddasa ta wurin ikonsu.
Sun kwanta tare da marasa kaciya tare da waɗanda aka kashe da takobi suna kuma
shan kunya tare da waɗanda suka gangara zuwa rami.
31 “Fir’auna, shi da dukan sojojinsa, za su gan su zai kuma ta’azantu domin dukan
jama’arsa da aka kashe da takobi, in ji Ubangiji Mai Iko Duka. 32 Ko da yake na sa ta
haddasa tsoro a ƙasar masu rai, Fir’auna da dukan jama’arsa za su kwanta a cikin
marasa kaciya, tare da waɗanda aka kashe da takobi, in ji Ubangiji Mai Iko Duka.”

# 33

*Ezekiyel mai tsaro*
*(Ezekiyel 3.16-21)*

1 Maganar Ubangiji ta zo mini cewa, 2 “Dan mutum, yi magana da mutanen ƙasarka
ka faɗa musu cewa, ‘Sa’ad da na kawo takobi a kan ƙasar, mutanen ƙasar kuwa suka
zaɓi ɗaya daga cikin mutanensu suka mai da shi mai tsaro, 3 ya kuma ga takobi yana
zuwa a kan ƙasar ya kuwa busa ƙaho don yă faɗakar da mutane, 4 in wani ya ji busar
amma bai kula ba, takobin zai zo ya ɗauki ransa, jininsa kuwa zai zauna a kansa.
5 Da yake ya ji ƙarar busar amma bai kula ba, jininsa zai zauna a kansa. Da a ce ya
kula, da ya ceci kansa. 6 Amma a ce mai tsaron ya ga takobi yana zuwa bai kuwa
busa ƙaho don yă faɗakar da mutane ba sai takobi ya zo ya ɗauki ran waninsu, za a
kawar da wannan mutum saboda zunubinsa, amma zan nemi hakkin jinin mutumin
a kan mai tsaron.’
7 “Dan mutum, na mai da kai mai tsaro bisa gidan Isra’ila; saboda haka ka ji
abin da zan faɗa ka kuma gargaɗe su. 8 Sa’ad da na ce wa mugu, ‘Ya mugun
mutum, tabbatacce za ka mutu,’ kai kuma ba ka yi magana don ka juyar da shi
daga hanyoyinsa ba, wannan mugun mutum zai mutu* domin zunubinsa, zan kuma
nemi hakkin jininsa a kanka. 9 Amma in ka faɗakar da mugun mutumin don yă juye

* **33:8** Ko kuwa ciki; haka ma a aya 9

daga hanyoyinsa bai kuwa yi haka ba, zai mutu saboda zunubinsa, amma kai za ka
kuɓutar da kanka.

*(Ezekiyel 18.21-30)*

10 “Ɗan mutum, faɗa wa gidan Isra’ila, ‘Ga abin da kuke cewa, “Laifofinmu da
zunubanmu suna nawaita mana, muna kuma lalacewa saboda† su. Ta ƙaƙa za mu
rayu?” ’ 11 Ka faɗa musu, ‘Muddin ina raye, in ji UBANGIJI Mai Iko Duka, ba na jin
daɗin mutuwar mugu, amma a maimako haka ya fi su juye daga hanyoyinsu su
rayu. Ku juye! Ku juye daga mugayen hanyoyinku! Don me za ku mutu, ya gidan
Isra’ila?’

12 “Saboda haka, ɗan mutum, ka faɗa wa mutanen ƙasarka, ‘Adalcin adali ba zai
cece shi sa’ad da ya ƙi yin biyayya ba, kuma muguntar mugu ba za tă sa ya fāɗi
sa’ad da ya juya daga gare ta ba. Adali, in ya yi zunubi, ba za a bari yă rayu saboda
adalcinsa na dā ba.’ 13 In na faɗa wa adali cewa tabbatacce zai rayu, amma sai ya
dogara ga adalcinsa ya kuma aikata mugunta, babu ayyukan adalcinsa da za a tuna;
zai mutu saboda muguntar da ya aikata. 14 Kuma in na ce wa mugu, ‘Tabbatacce za
ka mutu,’ amma sai ya juye daga zunubinsa ya kuma yi abin da yake gaskiya da kuma
daidai, 15 in ya mayar da jingina, ya mayar da abin da ya sata, ya kiyaye ƙa’idodin da
suke ba da rai, ya daina yin mugunta, tabbatacce zai rayu; ba zai mutu ba. 16 Babu
wani zunubin da ya aikata da za a tuna da shi. Ya yi abin da yake gaskiya da kuma
daidai; tabbatacce zai rayu.

17 “Duk da haka mutanen ƙasarka sun ce, ‘Hanyar Ubangiji ba daidai ba ce.’ Alhali
kuwa tasu ce ba daidai ba. 18 In adali ya juye daga adalcinsa ya yi mugunta, zai
mutu saboda haka. 19 Kuma in mugu ya juye daga muguntarsa ya aikata abin da
yake gaskiya da kuma daidai, zai rayu ta yin haka. 20 Duk da haka, ya gidan Isra’ila
kun ce, ‘Hanyar Ubangiji ba daidai ba ce.’ Amma zan hukunta kowane ɗayanku
gwargwadon ayyukansa.”

*An yi bayyanin fāɗuwar Urushalima*

21 A shekara ta goma sha biyu ta zaman bautanmu, a wata na goma a rana ta biyar,
wani mutumin da ya gudu daga Urushalima ya zo wurina ya ce, “Birnin ya fāɗi!”
22 To a yamman da ya wuce kafin mutumin ya iso, hannun UBANGIJI yana a kaina,
ya kuma buɗe bakina kafin mutumin ya iso wurina da safe. Sai bakina ya buɗu ban
kuma yi shiru ba.

23 Sai maganar UBANGIJI ta zo mini cewa, 24 “Ɗan mutum, mutanen da suke zama
a waɗannan kufai a ƙasar Isra’ila suna cewa, ‘Ibrahim mutum ɗaya ne kaɗai, duk
da haka Ibrahim ya mallaki ƙasar. Amma mu da muke da yawa; lalle an ba mu
ƙasar ta zama mallakarmu.’ 25 Saboda haka ka faɗa musu, ‘Ga abin da UBANGIJI
Mai Iko Duka yana cewa da yake kun ci nama da jini a cikinsa kuka kuma bauta
wa gumakanku kuka zub da jini, kuna gani za ku mallaki ƙasar? 26 Kun dogara ga
takobinku, kuka aikata abubuwan banƙyama, kowannenku kuma ya ƙazantar da
matar maƙwabcinsa. Kuna gani za ku mallaki ƙasar?’

27 “Ka faɗa musu wannan, ‘Ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa muddin
ina raye, waɗanda aka rage a kufai za su fāɗi ga takobi, waɗanda suke bayan gari
kuwa namun jeji za su cinye su, waɗanda suke a mafaka da kogwannin duwatsu
annoba za tă kashe su. 28 Zan mai da ƙasar kango, kuma fariyar ƙarfinta zai ƙare,
duwatsun Isra’ila za su zama kufai don kada wani ya ratsa su. 29 Sa’an nan za su
san cewa ni ne UBANGIJI, sa’ad da na mai da ƙasar kango saboda dukan abubuwan
banƙyamar da suka yi.’

30 “Game da kai kuma, ɗan mutum, mutanen ƙasarka suna magana da juna game
da kai a katanga da kuma ƙofofin gidaje, suna ce wa juna, ‘Ku zo mu tafi mu ji

† **33:10** Ko kuwa lalacewa a ciki

maganar da ta zo daga wurin UBANGIJI.' [31] Mutanena sukan zo wurinka, yadda suka
saba su zauna a gabanka don su saurari maganarka, amma ba sa aiki da abin da
suka ji. Da bakunansu suna nuna ƙauna, amma zukatansu cike da haɗama suke don
ƙazamar riba. [32] Tabbatacce, gare su ba ka fi mai waƙar ƙauna da murya mai daɗi
kana kuma yin kiɗa sosai ba, gama sukan ji maganarka amma ba sa amfani da ita.
[33] "Sa'ad da dukan wannan ya cika kuma zai cika ɗin, sa'an nan za su sani akwai
annabi a tsakiyarsu."

# 34

*Makiyaya da tumaki*

[1] Maganar UBANGIJI ta zo mini cewa, [2] "Ɗan mutum, ka yi annabci a kan makiyayan
Isra'ila; ka yi annabci ka ce musu, 'Ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa
kaiton makiyayan Isra'ila waɗanda suke kula da kansu ne kawai! Ashe, bai kamata
makiyaya ne su lura da tumaki ba? [3] Kuna cin kitsensu, kuna yi wa kanku tufafi da
gashinsu, kukan yanka turkakkun, amma ba ku yi kiwon tumakin ba. [4] Ba ku ƙarfafa
marasa ƙarfi ba, ko ku warkar da marasa lafiya ko ku ɗaura waɗanda suka ji rauni.
Ba ku dawo da waɗanda suka yi makuwa ko ku nemi waɗanda suka ɓace ba. Amma
sai kuka mallake su ƙarfi da yaji. [5] Saboda haka suka warwatse domin babu makiyayi,
kuma da suka warwatsu sai suka zama abincin namun jeji. [6] Tumakina suna ta yawo
a kan dukan duwatsu da kuma kowane tudu. Sun watsu a dukan duniya, kuma ba
wanda ya neme su.
[7] " 'Saboda haka, ku makiyaya, ku ji maganar UBANGIJI, [8] Muddin ina raye, in ji
UBANGIJI Mai Iko Duka, domin tumaki sun rasa makiyayi ta haka aka washe su
suka kuma zama abincin dukan namun jeji, kuma domin makiyayana ba su nemi
tumakina ba amma suka kula da kansu a maimakon tumakina, [9] saboda haka, ya ku
makiyaya, ku ji maganar UBANGIJI, [10] Ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa ina
gāba da makiyaya kuma zan nemi hakkin tumakina daga gare su. Zan hana su yin
kiwon tumakin don kada makiyayan su ƙara yin kiwon kansu. Zan ƙwace tumakina
daga bakunansu, ba kuwa za su ƙara zama abincinsu.
[11] " 'Gama ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa ni kaina zan nemi tumakina.
[12] Kamar yadda makiyayi yakan lura da tumakinsa da suka watse sa'ad da yake tare
da su, haka zan lura da tumakina. Zan cece su daga dukan wuraren da aka watsar
da su a ranar gizagizai da baƙin duhu. [13] Zan dawo da su daga al'ummai in kuma
tattara su daga ƙasashe, zan kuma kawo su cikin ƙasarsu. Zan yi kiwonsu a kan
duwatsun Isra'ila, a maɓulɓulai da kuma cikin wuraren zamansu a ƙasar. [14] Zan
kula da su a wurin kiwo mai kyau, kuma ƙwanƙolin duwatsun Isra'ila ne zai zama
wurin kiwonsu. Za su kwanta a wurin kiwo mai kyau, a can kuma za su yi kiwo
a wurin kiwo mai kyau a kan duwatsun Isra'ila. [15] Ni kaina zan lura da tumakina
in kuma sa su kwanta, in ji UBANGIJI Mai Iko Duka. [16] Zan nemi ɓatattuna in kuma
dawo da waɗanda suka yi makuwa. Zan ɗaura raunin waɗanda suka ji ciwo in kuma
ƙarfafa marasa ƙarfi, amma zan hallaka ƙarfafa da kuma masu ƙiba. Zan yi kiwo
tumaki da adalci.
[17] " 'Game da ku, tumakina, ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa zan
hukunta tsakanin tunkiya da tunkiya, da tsakanin raguna da awaki. [18] Bai isa ba a ce
kun yi kiwo a wuri mai kyau? Sai kun tattake sauran wurin kiwonku da ƙafafunku
tukuna? Bai isa ba a ce kun sha ruwa mai tsabta? Sai kun kuma gurɓata sauran da
ƙafafunku? [19] Dole ne tumakina su ci abin da kuka tattake su kuma sha abin da kuka
gurɓata da ƙafafunku?
[20] " 'Saboda haka ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka ya ce musu, duba, ni kaina zan
hukunta tsakanin turkakkun tumaki da ramammun tumaki. [21] Domin kun tunkuɗe

marasa ƙarfi da kafaɗunku, kun kuma tunkuye su da ƙahoninku sai da suka gudu,
[22] zan cece tumakina ba za su ƙara zama ganima ba. Zan hukunta tsakanin tunkiya
da tunkiya. [23] Zan sa musu makiyaya guda, bawana Dawuda, zai kuwa lura da su; zai
kula da su ya kuma zama makiyayinsu. [24] Ni UBANGIJI zan zama Allahnsu, bawana
kuma Dawuda zai zama yerima a cikinsu. Ni UBANGIJI na faɗa.

[25] " 'Zan yi alkawarin salama da su in kuma kawar wa ƙasar da namun jeji domin
su zauna a hamada su kuma kwana a kurmi lafiya lau. [26] Zan albarkace su in kuma
sa tuduna kewaye da su.* Zan zubo yayyafi a lokacinsa; za a kasance da yayyafin
albarka. [27] Itatuwan gona za su ba da 'ya'yansu, ƙasa kuma za tă ba da amfaninta;
mutane za su zauna lafiya a ƙasarsu. Za su san cewa ni ne UBANGIJI, sa'ad da na
karya karkiyarsu, na cece su daga hannun waɗanda suka bautar da su. [28] Ba za su
ƙara zama ganimar al'ummai ba, ba kuwa namun jeji za su cinye su ba. Za su zauna
lafiya, kuma babu wani da zai sa su ji tsoro. [29] Zan tanada musu ƙasar da aka sani
don hatsinta, ba za su kuma ƙara zama abin da yunwa za tă fara musu a ƙasa ba ko
su sha zargin sauran al'ummai. [30] Sa'an nan za su san cewa ni, UBANGIJI Allahnsu, ina
tare da su kuma cewa su, gidan Isra'ila, mutanena ne, in ji UBANGIJI Mai Iko Duka.
[31] Ku tumakina, tumakin wurin kiwona, mutanena ne, ni kuwa Allahnku ne, in ji
UBANGIJI Mai Iko Duka.' "

# 35

### *Annabci a kan Edom*

[1] Maganar UBANGIJI ta zo mini cewa, [2] "Dan mutum, ka fuskanci Dutsen Seyir; ka
yi annabci a kansa [3] ka ce, 'Ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa ina gāba da
kai, Dutsen Seyir, zan kuma miƙa hannuna gāba da kai in mai da kai kango. [4] Zan
mai da garuruwanka kufai za ka kuma zama kango. Sa'an nan za ka san cewa ni ne
UBANGIJI.

[5] " 'Domin ka riƙe ƙiyayya ta tun dā, ka kuma ba da mutanen Isra'ila domin a kashe
su da takobi a lokacin masifarsu, lokacin da adadin horonsu ya cika, [6] saboda haka
muddin ina raye, in ji UBANGIJI Mai Iko Duka, zan sa a zub da jininka zan kuwa fafare
ka. Da yake ba ka ƙi zub da jini ba, zub da jini zai fafare ka. [7] Zan mai da Dutsen
Seyir kango in kuma yanke dukan waɗanda suke shiga da fita a cikinka. [8] Zan cika
duwatsunka da matattu; waɗanda aka kashe da takobi za su fāɗi a kan tuddanka,
da cikin kwarurukanka, da cikin dukan kwazazzabanka. [9] Zan mai da kai kango
har abada; ba za a zauna a cikin garuruwanka ba. Sa'an nan za ka san cewa ni ne
UBANGIJI.

[10] " 'Domin kun ce, "Waɗannan al'ummai biyu da ƙasashe za su zama namu za
mu kuma mallake su," ko da yake Ni UBANGIJI ina a can, [11] saboda haka muddin ina
raye, in ji UBANGIJI Mai Iko Duka, zan sāka maka gwargwadon fushi da kuma kishin
da ka nuna a ƙiyayyarsu da ka yi zan kuma sanar da kaina a cikinsu sa'ad da na
hukunta ka. [12] Sa'an nan za ka san cewa Ni UBANGIJI na ji duk abubuwan banzan
da ka faɗa a kan duwatsun Isra'ila. Ka ce, "An mai da su kango an kuma ba mu su
mu cinye." [13] Ka yi fariya a kaina, ka kuma yi magana a kaina ba gaggautawa, na
ji shi sarai. [14] Ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa yayinda dukan duniya
take farin ciki, zan mai da kai kango. [15] Domin ka yi farin ciki sa'ad da gādon gidan
Isra'ila ya zama kufai, haka zan yi da kai, ya Dutsen Seyir, kai da dukan Edom. Sa'an
nan za ka san cewa ni ne UBANGIJI.' "

* **34:26** Ko kuwa zan mai da su da kuma wurare kewaye da tuduna su zama sanadin samun albarka

# 36

*Annabci wa duwatsun Isra'ila*

[1] "Dan mutum, ka yi annabci wa duwatsun Isra'ila ka ce, 'Ya duwatsun Isra'ila,
ku ji maganar UBANGIJI. [2] Ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa abokin gāba
yana magana game da ku cewa, "Yauwa! Tsofaffin tuddai sun zama mallakarmu
yanzu." ' [3] Saboda haka ka yi annabci ka ce, 'Ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana
cewa domin sun lalace ku suka kuma maishe ku kufai marar amfani a kowane gefe
saboda ku zama mallakar sauran al'ummai da kuma abin magana da tsegumi ga
mutane, [4] saboda haka, ya duwatsun Isra'ila, ku ji maganar UBANGIJI Mai Iko Duka,
ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana faɗa wa duwatsu da tuddai, wa kwazazzabai
da kwaruruka, wa kufai da garuruwan da suka zama kango waɗanda aka washe aka
wulaƙanta suka zama ganimar sauran al'ummai da suke kewaye da ku, [5] ga abin
da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa cikin kishina mai ƙuna na yi magana gāba da
sauran al'ummai, da kuma gāba da Edom, gama da farin ciki da reni a zukatansu
suka mai da ƙasata mallakarsu don su washe wuraren kiwonta.' [6] Saboda haka ka yi
annabci game da ƙasar Isra'ila ka kuma ce wa duwatsu da tuddai, wa kwazazzabai
da kwaruruka, 'Ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa ga shi, na yi magana
da kishina da hasalata saboda sun sha zargi wurin al'ummai. [7] Ga abin da UBANGIJI
Mai Iko Duka yana cewa na ɗaga hannuna sama na rantse cewa al'ummai da suke
kewaye da ku za su sha ba'a.

[8] " 'Amma ku, ya duwatsun Isra'ila, za ku miƙa rassanku ku ba da amfani ga
mutanena Isra'ila, gama ba da daɗewa ba za su komo gida. [9] Na damu da ku kuma
zan dube ku da tausayi; za ku nome ku kuma shuka, [10] zan kuma riɓaɓɓanya mutane
a kanku, dukan gidan Isra'ila ke nan. Za a zauna a birane a kuma sāke gina rusassun
wurare. [11] Zan sa mutane da dabbobi su yi yawa a kanku, za su kuma ba da 'ya'ya
su kuma yi yawa. Zan zaunar da mutane a kanku kamar dā zan kuma sa ku wadaita
fiye da dā. Sa'an nan za ku san cewa ni ne UBANGIJI. [12] Zan sa mutanena Isra'ila su
yi tafiya a kanku. Za su mallake ku, za ku kuma zama gādonsu; ba za ku ƙara sa su
rasa 'ya'yansu ba.

[13] " 'Ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa domin mutane suna magana
game da ku cewa, "Kun cinye mutane kuka kuma sa al'ummarku ta rasa 'ya'yanta,"
[14] saboda haka ba za ku ƙara cinye mutane ko ku sa al'ummarku ta rasa 'ya'ya ba,
in ji UBANGIJI Mai Iko Duka. [15] Ba zan ƙara bari ku ji maganar banza ta al'ummai ba,
ba kuwa za ku ƙara shan ba'ar mutane ko in sa al'ummarku ta fāɗi ba, in ji UBANGIJI
Mai Iko Duka.' "

*An tabbatar da maidowar Isra'ila*

[16] Maganar UBANGIJI ta sāke zuwa mini cewa, [17] "Dan mutum, sa'ad da mutanen
Isra'ila suke zama a ƙasarsu, sun ƙazantar da ita ta wurin halinsu da kuma
ayyukansu. Halinsu ya yi kamar rashin tsarkin mace a lokacin al'adarta a gabana.
[18] Saboda haka na husata da su domin sun yi kisankai a ƙasar kuma domin sun
ƙazantar da ita da gumakansu. [19] Na warwatsa su cikin al'ummai, suka kuwa
warwatsu cikin dukan ƙasashe; na hukunta su gwargwadon halinsu da ayyukansu.
[20] Kuma ko'ina da suka tafi a cikin al'ummai sun ɓata sunana mai tsarki, gama an
yi magana a kansu cewa, 'Waɗannan mutanen UBANGIJI ne, duk da haka dole su bar
ƙasarsa.' [21] Na damu saboda sunana mai tsarki, wanda gidan Isra'ila ya ɓata a cikin
al'ummai inda suka tafi.

[22] "Saboda haka ka faɗa musu cewa, 'Ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa
ba dominku ba ne, ya gidan Isra'ila da nake yin waɗannan abubuwa, amma saboda
sunana ne mai tsarki, wanda kuka ɓata a cikin al'ummai inda kuka tafi. [23] Zan nuna
tsarkin girman sunana, wanda aka ɓata a cikin al'umma, sunana da kuka ɓata a

cikinsu. Sa’an nan al’ummai za su san cewa ni ne Ubangiji, in ji Ubangiji Mai Iko
Duka, sa’ad da na nuna kaina mai tsarki ta wurinku a idanunsu.
24 “ ‘Gama zan fitar da ku daga al’ummai; zan tattara ku daga dukan ƙasashe in
komo da ku zuwa ƙasarku. 25 Zan yayyafa muku ruwa mai tsabta, zan kuwa tsarkake
ku daga dukan ƙazantarku daga kuma dukan gumakanku. 26 Zan ba ku sabuwa
zuciya in kuma sa sabon ruhu a cikinku; zan fid da zuciyar dutse in kuma ba ku
zuciyar nama. 27 Zan kuma sa Ruhuna a cikinku in kuma motsa ku ku bi ƙa’idodina
ku kuma kiyaye dokokina. 28 Za ku zauna a ƙasar da na ba wa kakanninku; za ku
zama mutanena, ni kuwa zan zama Allahnku. 29 Zan cece ku daga dukan rashin
tsabtarku. Zan sa hatsi ya yi yalwa ba zan kawo yunwa a kanku ba. 30 Zan ƙara
’ya’yan itatuwa da amfanin gona, saboda kada ku ƙara shan kunya a cikin al’ummai
saboda yunwa. 31 Sa’an nan za ku tuna mugayen hanyoyinku da mugayen ayyukanku,
za ku kuwa ji ƙyamar kanku saboda zunubanku da kuma ayyukanku na banƙyama.
32 Ina so ku san cewa ba na yi wannan saboda ku, in ji Ubangiji Mai Iko Duka. Ku ji
kunya ku kuma giggita saboda halinku, ya gidan Isra’ila!
33 “ ‘Ga abin da Ubangiji Mai Iko Duka yana cewa a ranar da na tsarkake ku daga
dukan zunubanku, zan sāke zaunar da ku a garuruwanku, a kuma sāke gina kufai.
34 Kasar da take kango a dā za ku nome ta a maimakon zama kango a idon dukan
masu ratsawa a cikinta. 35 Za su ce, “Wannan ƙasar da take kango a dā ta zama
kamar lambu Eden; biranen da dā suke kufai, kango da kuma aka lalata, yanzu suna
da katanga ana kuma zama a ciki.” 36 Sa’an nan al’ummai kewaye da ku da suka
rage za su san cewa Ni Ubangiji na sāke gina abin da aka lalace na kuma sāke shuka
abin da yake kango. Ni Ubangiji na faɗa, kuma zan aikata.’
37 “Ga abin da Ubangiji Mai Iko Duka yana cewa har yanzu zan ji roƙon gidan
Isra’ila in kuma yi musu wannan. Zan sa mutanensu su yi yawa kamar tumaki,
38 yawansu ya yi kamar garken tumaki don hadaya a Urushalima a ƙayyadaddun
lokuta bukukkuwarta. Haka biranen da suke kufai za su cika da ɗumbun mutane.
Sa’an nan za su san cewa ni ne Ubangiji.”

# 37

*Kwarin busassun ƙasusuwa*

1 Hannun Ubangiji yana a kaina, ya kuma fitar da ni ta wurin Ruhun Ubangiji ya
sa ni a tsakiyar kwarin; yana cike da ƙasusuwa. 2 Ya sa na kai na komo a ciki, na
kuma ga ƙasusuwa masu girma da yawa a ƙasar kwarin, ƙasusuwan da suka bushe
ƙwarai. 3 Sai ya tambaye ni cewa, “Ɗan mutum, waɗannan ƙasusuwa za su iya
rayu?”
Ni kuwa na ce, “Ya Ubangiji Mai Iko Duka, kai kaɗai ka sani.”
4 Sai ya ce mini, “Ka yi wa waɗannan ƙasusuwa annabci ka ce musu, ‘Busassun
ƙasusuwa, ku ji maganar Ubangiji! 5 Ga abin da Ubangiji Mai Iko Duka ya ce wa
waɗannan ƙasusuwa. Zan sa numfashi* ya shiga muku, za ku kuwa rayu. 6 Zan
harhaɗa muku jijiyoyi in sa muku tsoka in kuma rufe ku da fata; zan sa numfashi a
cikinku, za ku kuwa rayu. Sa’an nan za ku san cewa ni ne Ubangiji.’ ”
7 Saboda haka sai na yi annabci yadda aka umarce ni. Da nake annabcin, sai aka
ji motsi, ƙarar girgiza, sai ƙasusuwan suka harhaɗu, ƙashi ya haɗu da ƙashi. 8 Na
duba, sai ga jijiyoyi da nama suka bayyana a kansu fata kuma ta rufe su, amma ba
numfashi a cikinsu.
9 Sa’an nan ya ce mini, “Ka yi annabci wa numfashi; ka yi annabci, ɗan mutum, ka
ce masa, ‘Ga abin da Ubangiji Mai Iko Duka yana cewa ka fito daga kusurwoyi huɗu,

* **37:5** Ibraniyanci na wannan kalma zai iya zama iska ko ruhu (dubi ayoyi 6-14).

ya numfashi, ka kuma numfasa cikin waɗannan matattu, don su rayu.' " 10 Saboda
haka na yi annabci yadda aka umarce ni, sai numfashi ya shiga musu; suka rayu
suka kuma miƙe tsaye a ƙafafunsu babbar runduna ce ƙwarai.
11 Sa'an nan ya ce mini, "Dan mutum, waɗannan ƙasusuwa su ne dukan gidan
Isra'ila. Suna cewa, 'Kasusuwanmu sun bushe, sa zuciyarmu duk ya tafi; an share
mu ƙaf.' 12 Saboda haka yi annabci ka ce musu, 'Ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka
yana cewa ya mutanena, zan buɗe kaburburanku in fitar da ku daga cikinsu; zan mai
da ku ƙasar Isra'ila. 13 Sa'an nan ku, mutanena, za ku san cewa ni ne UBANGIJI, sa'ad
da na buɗe kaburburanku na fitar da ku daga cikinsu. 14 Zan sa Ruhuna a cikinku
za ku kuwa rayu, zan kuma zaunar da ku a ƙasarku. Sa'an nan za ku san cewa Ni
UBANGIJI na faɗa, zan kuma aikata, in ji UBANGIJI.' "

### *Al'umma ɗaya a ƙarƙashin sarki guda*

15 Maganar UBANGIJI ta zo mini cewa, 16 "Dan mutum, ka ɗauki sanda ka rubuta
a kansa, 'Na Yahuda da Isra'ilawan da suke tare da shi.' Sa'an nan ka ɗauki wani
sanda, ka rubuta a kansa, 'Sandan Efraim, na Yusuf da dukan gidan Isra'ilan da suke
tare da shi.' 17 Ka haɗa su su zama sanda guda saboda su kasance ɗaya a hannunka.
18 "In mutanen ƙasarka suka tambaye ka cewa, 'Ba za ka faɗa mana abin da kake
nufi da wannan ba?' 19 Ka ce musu, 'Ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa,
Zan ɗauki sandan Yusuf, wanda yake a hannun Efraim, da na kabilan Isra'ilawan
da suke tare da shi, in haɗa shi da sandan Yahuda, in mai da su sanda guda, za su
kuwa zama ɗaya a hannuna.' 20 Ka riƙe sandunan da ka yi rubutun a gabansu 21 ka
ce musu, 'Ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa zan fitar da Isra'ilawa daga
al'ummai inda suka tafi. Zan tattara su daga dukan kewaye in komo da su ƙasarsu.
22 Zan mai da su al'umma ɗaya a cikin ƙasar, a kan duwatsun Isra'ila. Za a kasance
da sarki guda a kan dukansu ba za su ƙara zama al'ummai biyu ko su rabu su zama
masarautai biyu ba. 23 Ba za su ƙara ƙazantar da kansu da gumaka da mugayen
siffofi ko kuma da wani daga laifofinsu ba, gama zan cece su daga dukan zunubinsu
na ridda, zan kuma tsarkake su. Za su zama mutanena, ni kuma zan zama Allahnsu.
24 " 'Bawana Dawuda zai zama sarki a kansu, dukansu kuwa za su kasance da
makiyayi guda. Za su bi dokokina su kuma kiyaye ƙa'idodina. 25 Za su zauna a ƙasar
da na ba wa bawana Yaƙub, ƙasar da kakanninsu suka zauna. Su da 'ya'yansu
da 'ya'ya 'ya'yansu za su zauna a can har abada, kuma Dawuda bawana zai zama
sarkinsu har abada. 26 Zan yi alkawarin salama da su; zai zama madawwamin
alkawari. Zan kafa su in ƙara yawansu, zan kuma sa wuri mai tsarkina a cikinsu
har abada. 27 Mazaunina zai kasance da su; zan kuwa zama Allahnsu, za su kuma
zama mutanena. 28 Sa'an nan al'ummai za su san cewa Ni UBANGIJI na mai da Isra'ila
mai tsarki, sa'ad da wuri mai tsarkina yana a cikinsu har abada.' "

# 38

### *Annabci a kan Gog*

1 Maganar UBANGIJI ta zo mini cewa, 2 "Dan mutum, ka fuskanci Gog, na ƙasar
Magog, babban sarkin* Meshek da Tubal; ka yi annabci a kansa 3 ka ce, 'Ga abin da
UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa ina gāba da kai, ya Gog, babban sarkin† Meshek
da Tubal. 4 Zan juyar da kai, in sa ƙugiyoyi a muƙamuƙanka in fitar da kai tare
da dukan sojojinka, dawakanka, mahayan dawakanka saye da makamai, da kuma
jama'a mai girma masu riƙe da garkuwoyi manya da ƙanana, dukansu da takuba
a zāre. 5 Farisa, Kush‡ da Fut za su kasance tare da su, duka riƙe da garkuwoyi

* **38:2** Ko kuwa sarkin Rosh, † **38:3** Ko kuwa sarkin Rosh, ‡ **38:5** Wato, yankin Nilu na Bisa

da hulunan kwano, 6 haka ma Gomer da dukan sojojinsa, da Bet Togarma daga can
arewa tare da dukan sojojinsa, alʼummai masu yawa tare da kai.
7 “ ʻKa shirya; ka kintsa, kai da dukan jamaʼarka da suka taru kewaye da kai,
ka kuma zama mai ba su umarni. 8 Bayan kwanaki masu yawa za a kira ka. A
shekaru masu zuwa za ka kai hari a ƙasar da ta farfaɗo daga yaƙi, wadda aka tattara
mutanenta daga alʼummai masu yawa zuwa duwatsun Israʼila, dā kango ne sosai. An
fitar da su daga alʼummai, yanzu kuwa dukansu suna zama lafiya. 9 Kai da dukan
sojojinka da kuma alʼummai masu yawa da suke tare da kai za ku haura, kuna cin
gaba kamar hadari; za ku zama kamar girgijen da yake rufewa ƙasa.
10 “ ʻGa abin da Ubangiji Mai Iko Duka yana cewa a ranar, tunani zai shiga cikin
zuciyarka za ka kuma ƙirƙiro muguwar dabara. 11 Za ka ce, “Zan kai hari wa ƙasar da
ƙauyukanta ba su da katanga; zan fāɗa wa mutanen da suke zamansu kurum cikin
salama, dukansu suna zama babu katanga babu ƙofofi ko ƙyamare. 12 Zan washe in
kwashe ganima in kuma juye hannuna gāba da kufai da aka sāke zaunar da mutanen
da aka tattara daga alʼummai, masu yawan shanu da kayayyaki, masu zama a tsakiyar
ƙasa.” 13 Sheba da Dedan da ʼyan kasuwar Tarshish da dukan ƙauyukanta§ za su ce
maka, “Ka zo ka kwashe ganima ne? Ka tattara jamaʼarka don ka yi waso, ka kuma
kwashe azurfa da zinariya, ka kwashe shanu da kayayyaki ka kuma ƙwace ganima
mai yawa?” ʼ
14 “Saboda haka ɗan mutum, ka yi annabci ka ce wa Gog, ʻGa abin da Ubangiji Mai
Iko Duka yana cewa a ranar, saʼad da mutanena Israʼila suna zaman lafiya, ba za ka
sani ba? 15 Za ka zo daga wurinka a can arewa, kai da alʼummai masu yawa tare
da kai, dukansu suna hawan dawakai, jamaʼa mai yawa, babbar runduna. 16 Za ka
ci gaba a kan mutanena Israʼila kamar yadda girgijen yakan rufe ƙasa. A kwanaki
masu zuwa, ya Gog, zan kawo ka, ka yi yaƙi da ƙasata, domin alʼummai su san ni
saʼad da na nuna kaina mai tsarki ta wurinka a gabansu.
17 “ ʻGa abin da Ubangiji Mai Iko Duka yana cewa ba kai ba ne na yi magana da
kai a kwanakin dā ta wurin bayina annabawan Israʼila? A lokacin sun yi annabci
shekaru masu yawa cewa zan kawo ka, ka yaƙe su. 18 Ga abin da zai faru a ranar.
Saʼad da Gog ya fāɗa wa ƙasar Israʼila, fushina mai zafi zai ƙuna, in ji Ubangiji Mai
Iko Duka. 19 Cikin kishina da hasalata mai zafi zan furta cewa a wannan lokaci za a
yi babbar girgizar ƙasa a ƙasar Israʼila. 20 Kifin teku, tsuntsayen sarari, namun jeji,
kowace halitta mai rarrafe da kuma dukan mutane a duniya za su yi rawar jiki a
gabana. Za a tumɓuke duwatsu, a ragargaza tsaunuka, kuma kowane bango zai fāɗi
ƙasa. 21 Zan kira takobi a kan Gog a dukan duwatsuna, in ji Ubangiji Mai Iko Duka.
Kowane takobin mutum zai yi gāba da ɗanʼuwansa. 22 Zan yi hukunci a kansa da
annoba da kuma zub da jini; zan yi ruwa mai yawa da ƙanƙara da kibiritu mai cin
wuta a kansa da a kan sojojinsa da kuma a kan alʼummai masu yawa da suke tare
da shi. 23 Ta haka zan nuna girmana da kuma tsarkina, zan sanar da kaina a gaban
alʼummai masu yawa. Saʼan nan za su san cewa ni ne Ubangiji.ʼ

# 39

1 “Ɗan mutum, ka yi annabci a kan Gog ka ce, ʻGa abin da Ubangiji Mai Iko Duka
yana cewa ina gāba da kai, ya Gog, babban sarkin* Meshek da Tubal. 2 Zan juya ka
in kuma ja ka. Zan kawo ka daga can arewa in aike ka don ka fāɗa wa duwatsun
Israʼila. 3 Saʼan nan zan karya bakan da take a hannun hagunka, in sa kibiyoyin da
suke a hannun damanka su fāɗi. 4 A kan duwatsun Israʼila za ka fāɗi, kai da sojojinka
da kuma alʼummai da suke tare da kai. Zan bayar da kai ka zama abinci ga tsuntsaye

§ **38:13** Ko kuwa zakokinta masu ƙarfi * **39:1** Ko kuwa Gog, sarkin Rosh,

da namun jeji masu cin nama. 5 Za ka mutu a fili, gama haka ni na faɗa, in ji Ubangiji
Mai Iko Duka. 6 Zan aika da wuta a kan Magog da kuma a kan waɗanda suke zama
lafiya a bakin teku, za su kuwa san cewa ni ne Ubangiji.
7 “ ‘Zan sanar da sunana mai tsarki a cikin mutanena Isra’ila. Ba zan ƙara bari a
ɓata sunana mai tsarki ba, kuma al’ummai za su san cewa Ni Ubangiji Mai Tsarki ne
a cikin Isra’ila. 8 Yana zuwa! Tabbatacce zai faru, in ji Ubangiji Mai Iko Duka. Ranar
da na yi magana ke nan.
9 “ ‘Sa’an nan waɗanda suke zama a garuruwan Isra’ila za su fita su tattara
makamai su hura wuta da su su kuma ƙone su, manya da ƙanana garkuwoyi,
bakkuna da kibiyoyi, kulake da māsu. Shekara bakwai za su yi amfani da su don
hura wuta. 10 Ba za su yi wahalar zuwa jeji don neman itacen hura wuta ba, domin
za su yi amfani da makamai don hura wuta. Za su kuma washe waɗanda suka washe
su ganima, in ji Ubangiji Mai Iko Duka.
11 “ ‘A ranar zan yi wa Gog makabarta a cikin Isra’ila, a kwarin waɗanda suke
tafiya wajen gabashin Teku. Za tă tare hanyar matafiya, domin za a binne Gog da
dukan mutanensa a can. Ta haka za a kira wurin Kwarin Haman Gog.†
12 “ ‘Watanni bakwai gidan Isra’ila zai yi ta binne su don a tsarkake ƙasar. 13 Dukan
mutanen ƙasar za su binne su, kuma ranar da za a ɗaukaka ni za tă zama ranar tuni
a gare su, in ji Ubangiji Mai Iko Duka.
14 “ ‘Za a ɗauki mutane kullum don tsabtacce ƙasar. Waɗansu za su ratsa ƙasar,
ƙari da waɗannan, waɗansu za su binne gawawwakin da suka ragu a ƙasar. A
ƙarshen watanni bakwai ɗin za su fara bincikensu. 15 Yayinda suke ratsa ƙasar, in
waninsu ya ga ƙashin mutum, zai kafa shi kamar alama a gefe sai masu haƙa kabari
sun binne shi a Kwarin Haman Gog. 16 Akwai wani garin da ake kira Hamona‡ zai
kasance a can. Ta haka za su tsabtacce ƙasar.’
17 “Dan mutum, ga abin da Ubangiji Mai Iko Duka yana cewa, ka gayyato kowane
irin tsuntsu da dukan namun jeji, ‘Ku taru ku kuma zo wuri ɗaya daga ko’ina don
hadayar da nake shirya muku, babbar hadaya a kan duwatsun Isra’ila. A can za
ku ci nama ku kuma sha jini. 18 Za ku ci naman manyan mutane ku kuma sha
jinin sarakunan duniya sai ka ce an yanka raguna da ’yan tumaki, awaki da bijimai,
dukansu turkakkun dabbobi daga Bashan. 19 A hadayar da nake shirya muku, za
ku ci kitse sai kun ƙoshi ku kuma sha jini sai kun bugu. 20 A teburina za ku ci iya
ƙoshiyarku da naman jama’a da kuma mahaya, manyan mutane da sojoji na kowane
iri,’ in ji Ubangiji Mai Iko Duka.
21 “Zan nuna ɗaukakata a cikin al’ummai, kuma dukan al’ummai za su ga hukuncin
da zan yi da kuma hannu mai nauyin da zan ɗora a kansu. 22 Daga wannan rana
zuwa gaba gidan Isra’ila zai san cewa ni ne Ubangiji Allahnsu. 23 Al’ummai kuma za
su san cewa mutanen Isra’ila sun tafi zaman bauta saboda zunubinsu, domin sun yi
rashin aminci gare ni. Saboda haka na kawar da fuskata daga gare su na miƙa su
ga abokan gābansu, suka kuwa mutu ta takobi. 24 Na yi da su gwargwadon rashin
tsabtarsu da laifofinsu, na kuma kawar da fuskata daga gare su.
25 “Saboda haka ga abin da Ubangiji Mai Iko Duka yana cewa zan komo da Yaƙub
daga zaman bauta§ zan kuma yi wa dukan Isra’ila jinƙai, zan kuma yi kishi saboda
sunana mai tsarki. 26 Za su manta da kunyar da suka sha da dukan rashin amincin
da suka nuna mini sa’ad da suke zama lafiya a ƙasarsu inda ba wanda zai tsorata
su. 27 Sa’ad da na komo da su daga al’ummai na kuma tattara su daga ƙasashen
abokan gābansu, zan nuna kaina mai tsarki ta wurinsu a gaban al’ummai masu
yawa. 28 Sa’an nan za su san cewa ni ne Ubangiji Allahnsu, gama ko da yake na tura

† **39:11** Haman Gog yana nufin mutanen Gog. ‡ **39:16** Hamona yana nufin jama’a. § **39:25** Ko kuwa yanzu
mai da nasarar Yaƙub

su zaman bauta a cikin al'ummai, zan tattara su zuwa ƙasarsu, ba tare da barin wani
a baya ba. 29 Ba zan ƙara kawar da fuskata daga gare su, gama zan zuba Ruhuna a
kan gidan Isra'ila, in ji Ubangiji Mai Iko Duka."

# 40

### *Wurin sabon haikali*

1 A shekara ta ashirin da biyar ta zaman bauta, a farkon shekara, a rana ta goma
ga wata, a shekara ta goma sha huɗu bayan fāɗuwar birnin Urushalima, a wannan
rana ikon Ubangiji ya sauko a kaina ya kuma iza ni. 2 Cikin wahayin, Allah ya kai
ni ƙasar Isra'ila ya sa ni a kan wani dutse mai tsayi ƙwarai, inda a gefen kudunsa
akwai gine-ginen da suka yi kamar birni. 3 A cikin wahayin ya kai ni can, na kuma ga
mutum wanda kamanninsa ya yi kamar tagulla; yana tsaye a hanyar shiga yana riƙe
da igiyar lilin da kuma karan awo a hannunsa. 4 Mutumin ya ce mini, "Ɗan mutum,
duba da idanunka, ka ji da kunnuwanka ka kuma lura da kowane abin da zan nuna
maka, gama abin da ya sa na kawo ka nan ke nan. Ka faɗa wa gidan Isra'ila duk
abin da ka gani."

### *Kofar shiga ta gabas zuwa filin waje*

5 Na ga katanga da ya kewaye filin haikali gaba ɗaya. Tsawon karan awon da yake
a hannun mutumin kamu shida ne, sai ya auna kaurin katangar ya sami kamu shida,
tsayinta kuma kamu shida.
6 Sa'an nan ya tafi ƙofar da take fuskantar gabas. Ya hau matakanta ya auna
madogarar ƙofa; zurfinta kamu shida ne. 7 Tsawon kowane ɗakin matsara kamu
shida ne, fāɗinsa kuma kamu shida, kaurin bangayen da suka raba ɗaki da ɗaki
kamu biyar ne. Zurfin madogarar ƙofar da yake dab da shirayin da yake fuskantar
haikalin kamu shida ne.
8 Sa'an nan ya auna shirayin hanyar shiga; 9 zurfinsa kamu takwas ne, kaurin
kowane madogarar ƙofarsa kuwa kamu biyu ne. Shirayi hanyar shiga yana fuskantar
haikalin.
10 A cikin ƙofar gabas akwai ɗakuna uku a kowane gefe na hanyar shiga; dukan
ukun girmansu ɗaya, bangayen da suke tsakani a kowane gefe girmansu ɗaya ne.
11 Sa'an nan ya auna bakin hanyar shiga ya sami fāɗinsa kamu goma, tsawonsa
kuma kamu goma sha uku. 12 A gaban kowane ɗakin akwai bango mai tsayi kamu
ɗaya, ɗakunan kuma kamu shida-shida ne a kowane gefe. 13 Sa'an nan ya auna
hanyar shiga daga saman bangon ɗaki a baya zuwa saman ɗakin da yake ɗaura da
shi; nisansu kamu ashirin da biyar ne daga bango zuwa bango. 14 Ya auna ɗakin
bakin ƙofa na can ƙarshen hanyar shiga ya sami kamu sittin. Awon ya kai har zuwa
shirayin* da yake fuskantar filin.† 15 Nisan da take daga mashigin hanyar shiga zuwa
can ƙarshen shirayin, kamu hamsin ne. 16 Akwai ƙananan tagogi a ɗakunan da
kuma a bangayen hanyar shiga, yadda suke a shirayin; tagogi a kewaye duka suna
fuskantar ciki. An yi wa bangayen da suke waje ƙofar shiga ado da zāne-zāne siffofin
itatuwan dabino.

### *Filin waje*

17 Sai mutumin ya bi da ni ta hanyar shiga zuwa filin waje, inda na ga ɗakuna
talatin da aka gina kewaye a filin waje na filin. An gina waɗannan ɗakunan gefe
a jikin bangon waje, a gabansu kuwa akwai daɓe kewaye da filin. 18 Daɓen ya bi
ta daidai gefen hanyoyin shiga, kuma faɗinsa ya yi daidai da tsawon ƙofofin shiga;
wannan shi ne daɓen da yake ƙasa-ƙasa.

---

* **40:14** Seftuwajin; Ibraniyanci bangon † **40:14** Ma'anar Ibraniyanci na wannan aya dai babu tabbas.

19 Sa'an nan ya auna nisan da take daga hanyar shiga da take ƙasa-ƙasa daga ciki
zuwa waje na filin ciki; ya kai kamu ɗari a gefen gabas haka ma yake a gefen arewa.

### *Kofar arewa*

20 Sa'an nan mutumin ya auna tsawo da fāɗin ƙofar da take fuskantar arewa,
wadda take bi zuwa filin waje. 21 Kofar shigar ma tana da ɗakuna uku-uku a kowane
gefe. Girman bangayen da suka miƙe, da kuma shirayinta daidai suke da na ƙofa
ta fari. Tsawonta kamu hamsin, fāɗinta kuwa kamu ashirin da biyar. 22 Tagoginta,
shirayinta da siffofin itatuwan dabinon da aka yi zāne-zānen adonta duk girmansu
ɗaya ne da na ƙofar da take fuskantar gabas. Ɗakin shiga shi ma ya fuskanci filin
yana kuma da matakai bakwai waɗanda suka bi zuwa ƙofar shiga, da shirayinta
ɗaura da su. 23 Akwai ƙofa zuwa filin ciki wadda take fuskantar ƙofar arewa, kamar
dai yadda take a gabas. Ya auna daga ƙofa zuwa ƙofar da take ɗaura ta ita; ya sami
kamu ɗari.

### *Kofar kudu*

24 Sa'an nan ya kai ni gefen kudu, na kuma ga ƙofa tana fuskantar kudu. Ya auna
madogaranta da shirayinta, dukansu girmansu ɗaya ne kamar sauran ƙofofi biyun.
25 Hanyar shiga da shirayinta suna da tagogi duk a kewaye, kamar tagogin sauran.
Tsawonta kamu hamsin ne fāɗinta kuma kamu ashirin da biyar ne. 26 Matakai
bakwai sun haura zuwa ƙofar, da shirayi ɗaura da matakan; tana da zāne-zānen
adon itatuwan dabino a bangayen a kowane gefe. 27 Filin cikin ma yana da ƙofar da
ta fuskanci kudu, sai ya auna daga wannan ƙofa zuwa ƙofar waje a gefen kudu; ya
sami kamu ɗari.

### *Kofofin zuwa filin ciki*

28 Sai ya kawo ni cikin filin ciki ta ƙofar kudu, ya kuma auna ƙofar kudu; ita ma
tana da girma ɗaya da sauran ƙofofin shiga. 29 Ɗakunanta na matsara, bangayenta
duk suna da girma ɗaya da sauran. Hanyar shiga da shirayinta suna da tagogi duk
a kewaye. Tsawonta kamu hamsin ne, fāɗinta kuma kamu ashirin da biyar ne.
30 (Fāɗin shirayun hanyoyin shiga kewaye da filin ciki kamu ashirin da biyar ne,
fāɗinsu kuma kamu biyar.) 31 Shirayin ƙofar yana fuskantar filin waje; an yi zāne-
zānen adon itatuwan dabino a madogarar bangayen hanyar shiga. Yana kuma da
matakai takwas.
32 Sai ya kai ni filin da yake ciki a gefen gabas, ya kuma auna hanyar shiga;
girmanta iri ɗaya ne kamar sauran. 33 Ɗakunanta, bangayenta da shirayinta duk
girmansu iri ɗaya ne kamar sauran. Hanyar shiga da shirayinta suna da tagogi duk a
kewaye. Tsawon hanyar shiga kamu hamsin ne, fāɗinta kuma kamu ashirin da biyar.
34 Shirayinta yana fuskantar filin da yake waje; tana da zāne-zānen adon itatuwan
dabino a madogararta. Tana kuma da matakai takwas.
35 Sa'an nan ya kawo ni ƙofar arewa ya kuma auna ta. Girmanta ɗaya ne da sauran,
36 Haka ma ɗakunanta, bangayenta da shirayinta, ƙofar tana da tagogi duk a kewaye.
Tsawonta kamu hamsin, fāɗinta kuma kamu ashirin da biyar. 37 Shirayin ƙofar‡
ta fuskanci filin waje; tana da zāne-zānen adon itatuwan dabino a madogaranta,
matakai takwas kuwa sun haura zuwa wajenta.

### *Ɗakuna don shirya hadayu*

38 Ɗakin da hanya ta ratsa ciki yana kusa da shirayin a kowane hanyoyin shiga na
ciki, inda a kan wanke hadayun ƙonawa. 39 A shirayin hanyar shiga akwai tebur biyu
a kowane gefe, inda ake yankan hadayun ƙonawa, hadayun zunubi da kuma hadayun
laifi. 40 Ta bangon waje na shirayin hanyar shiga, kusa da matakai a mashigin zuwa

‡ **40:37** Seftuwajin (dubi kuma ayoyi 31 da 34); Ibraniyanci madogarar

hanyar shiga da take arewa akwai tebur biyu, akwai kuma tebur biyu a gefe ɗaya na
matakan. 41 Duka dai akwai tebur huɗu a gefe ɗaya na hanyar shiga, huɗu kuma a
ɗaya gefen, tebur takwas ke nan gaba ɗaya, inda a kan yanka hadayu a kai. 42 Akwai
kuma tebur huɗu da aka yi da sassaƙaƙƙun duwatsu don hadayun ƙonawa, tsawon
kowanne kuwa kamu ɗaya da rabi ne, fāɗinsa kamu ɗaya da rabi, tsayinsa kuma
kamu ɗaya. A kansu ne a kan ajiye kayan yanka hadayun ƙonawa da kuma sauran
hadayu. 43 Aka kakkafa ƙugiyoyi kewaye a bangon, tsawon kowanne ya yi fāɗin tafin
hannu. An yi amfani da teburin don a riƙa ajiye naman hadayu.

### *Ɗakuna domin firistoci*

44 Waje da ƙofar ciki, a cikin filin ciki, akwai ɗakuna biyu, ɗaya§ a gefen ƙofar
arewa yana kuma fuskantar kudu, wani kuma a gefen ƙofar kudu* yana fuskantar
arewa. 45 Sai mutumin ya ce mini, "Ɗakin da yake fuskantar kudu ne na firistocin
da suke lura da haikali, 46 ɗaya ɗakin kuma da yake fuskantar arewa ne na firistocin
da suke lura da bagade. Waɗannan su ne 'ya'yan Zadok maza, waɗanda su ne kaɗai
Lawiyawan da za su iya yin kusa da UBANGIJI don su yi hidima a gabansa."
47 Sa'an nan ya auna filin, murabba'i ne, tsawonsa kamu ɗari, fāɗinsa kuma kamu
ɗari. Bagaden kuwa yana a gaba a cikin haikalin.

### *Haikalin*

48 Sai ya kawo ni shirayin haikalin ya kuma auna madogaran shirayin; fāɗinsu
a kowane gefe kamu biyar-biyar ne. Fāɗin mashigin kamu goma sha huɗu ne,
bangayenta† kuma kamu uku-uku ne a kowane gefe. 49 Fāɗin shirayin kamu ashirin
ne, kamu goma sha biyu‡ kuma daga gaba zuwa baya. A kan kai samansa ta wurin
hawan matakai,§ akwai kuma ginshiƙai a kowane gefe na madogaran.

## 41

1 Sai mutumin ya kawo ni wuri mai tsarki da yake waje ya kuma auna
madogaransa; fāɗin gefe-gefen kamu shida ne a kowane gefe. 2 Faɗin ƙofar shiga
kamu goma ne, fāɗin bangaye a kowane madogararta kamu biyar-biyar ne. Ya kuma
auna wuri mai tsarkin da yake waje; tsawonsa kamu arba'in fāɗinsa kuma kamu
ashirin.
3 Sa'an nan ya shiga wuri mai tsarki da yake can ciki ya auna madogarar ƙofar
shigar; fāɗin kowanne kamu biyu ne. Faɗin ƙofar shigan kamu shida ne, fāɗin
bangayen a kowane gefenta kamu bakwai-bakwai ne. 4 Ya kuma auna tsawon wuri
mai tsarki da yake can ciki; tsawon kamu ashirin ne, fāɗinsa kuma kamu ashirin
daga ƙurewa wuri mai tsarki da yake waje. Ya ce mini, "Wannan shi ne Wuri Mafi
Tsarki."
5 Sa'an nan ya auna bangon haikalin; kaurinsa kamu shida ne, kuma kowane ɗakin
da yake a gefe kewaye da haikalin fāɗinsa kamu huɗu ne. 6 Ɗakunan da suke gefe
masu hawa uku ne, wani bisa wani, guda talatin a kowane hawa. Akwai katanga
kewaye da bangayen haikalin don ta tokare ɗakunan, domin ba a so ɗakunan su
jingina da bangon haikalin. 7 Faɗin ɗakunan da suke gefe kewaye da haikalin ya
yi ta ƙaruwa daga hawa zuwa hawa. Ginin da aka yi kewaye da haikalin ya yi ta
ƙaruwa daga hawa zuwa hawa, don haka ɗakunan suka yi ta ƙara fāɗi yayinda suka
ƙara bisa. Akwai mataki daga ɗaki na ƙasa zuwa ɗaki na bisa ta hanya hawa ɗaki
na tsakiya.

---

§ **40:44** Seftuwajin; Ibraniyanci ɗakuna don mawaƙa, waɗanda suke * **40:44** Seftuwajin; Ibraniyanci gabas
† **40:48** Seftuwajin; Ibraniyanci bakin ƙofar take ‡ **40:49** Seftuwajin; Ibraniyanci goma sha ɗaya § **40:49**
Ibraniyanci; Seftuwajin Matakai goma suka haura zuwa wurinsa

8 Na ga cewa haikalin yana da ɗagaggen tushe kewaye da shi, wanda ya zama
harsashin ɗakunan da suke gefe. Tsawonsa kara guda ne mai tsawon kamu shida.
9 Kaurin bangon waje na ɗakunan da suke gefe kamu biyar ne. Faɗin filin da yake
tsakanin ɗakunan da suke gefen haikalin 10 da ɗakunan firistoci kamu ashirin ne
kewaye da haikalin. 11 Akwai ƙofofin shiga daga fili, ɗaya a arewa ɗaya kuma a
kudu; fāɗin tushen da ya yi kusa da filin kamu biyar ne kewaye.

12 Faɗin ginin da yake fuskantar filin haikali a wajen yamma kamu saba'in ne.
Kaurin bangon ginin kamu biyar ne kewaye, tsawonsa kuma kamu tasa'in ne.

13 Sa'an nan ya auna haikalin; tsawonsa kamu ɗari ne, tsawon filin haikalin da
ginin tare da bangayensa su ma kamu ɗari ne. 14 Faɗin filin haikalin a wajen gabas,
haɗe da gaban haikalin, kamu ɗari ne.

15 Sa'an nan ya auna tsawon ginin da yake fuskantar filin a bayan haikalin, haɗe
da rumfunansa a kowane gefe, kamu ɗari.

Wuri mai tsarki da yake waje, wuri mai tsarki da yake can ciki da shirayin da yake
fuskantar filin, 16 da madogaran ƙofa da matsattsun tagogi da rumfuna kewaye da
su ukun, har da kome da yake gaba haɗe da madogarar ƙofa, an rufe su da katako.
An rufe bangon haikalin daga ƙasa har zuwa tagogi, tagogin kuwa an rufe su. 17 A
filin da yake bisan ƙofar shiga na waje zuwa wuri mai tsarki na can ciki da kuma
a bangayen da aka daidaita tsakani kewaye da wuri mai tsarki na can ciki da kuma
na can waje 18 an zāna siffofin kerubobi da na itatuwan dabino. Zānen siffar itacen
dabino yana a tsakanin kerub da kerub. Kowane kerub yana da fuska biyu, 19 fuskar
ɗaya kamar ta mutum tana fuskantar zānen siffar itacen dabino a wannan gefe, ɗaya
fuskar kamar ta zaki tana fuskantar zānen siffar itacen dabino na wancan gefe. Haka
aka zāna su dukan a jikin bangon haikalin kewaye. 20 Daga ƙasa zuwa daurin ƙofa,
an zāna siffofin kerubobi da na itatuwan dabino a waje na wuri mai tsarki.

21 Wuri mai tsarki da yake waje yana da madogarar ƙofa murabba'i, haka ma
wadda take a gaban Wuri Mafi Tsarki. 22 Akwai bagaden katako mai tsayi kamu uku,
fāɗinsa kamu biyu da kuma tsawonsa kamu biyu; kusurwansa, tushensa da kuma
gefe-gefensa duk katako ne. Sai mutumin ya ce mini, "Wannan shi ne tebur da yake
a gaban Ubangiji." 23 A wuri mai tsarki da yake waje da kuma Wuri Mafi Tsarki suna
da ƙofa biyu a haɗe. 24 Kowace ƙofa tana da murfi biyu masu buɗewa ciki da waje.
25 A ƙofofin wuri mai tsarki da yake waje an zāna siffofin kerubobi da na itatuwan
dabino kamar yadda aka zāna a bangayen, akwai kuma rumfar da aka yi da itace a
gaban shirayin. 26 A bangayen da suke gefen shirayin akwai matsattsun tagogi da aka
zāna siffar itatuwan dabino a kowane gefe. Gefe-gefen ɗakunan haikalin ma suna
da rumfuna.

# 42

*Dakuna don firistoci*

1 Sai mutumin ya kai ni wajen arewa zuwa cikin filin da yake waje ya kuma kawo
ni ɗakunan da suke ɗaura da filin haikalin da yake a gefen arewa. 2 Tsawon ginin
da yake fuskantar arewa kamu ɗari ne fāɗinsa kuma kamu hamsin. 3 A gaban kamu
ashirin na filin da yake can ciki da kuma a gaban daɓen filin da yake waje, akwai
rumfuna a jere waɗanda suke fuskantar juna hawa uku-uku. 4 A gaban ɗakunan
akwai hanya a can ciki mai fāɗin kamu goma, tsawonta kuma kamu ɗari. Kofofinsu
suna wajen arewa. 5 Dakunan da suke bisa ba su da fāɗi, gama mataki hawan benen
ya cinye wuri fiye da a ɗakunan da suke a hawa na ƙasa da na tsakiya. 6 Dakunan da
suke a hawa na uku ba su da ginshiƙai, yadda filayen suka kasance da su, saboda haka
suka matsu fiye da waɗanda suke a hawa na ƙasa da na tsakiya. 7 Akwai katanga
wadda take waje, wadda ta yi hannun riga da ɗakunan filin waje; ta miƙe a gaban

ɗakunan, tsawonta kamu hamsin ne. 8 Yayinda tsawon jerin ɗakunan da suke a gefe
kusa da filin da yake waje kamu hamsin ne, tsawon jerin ɗakunan da suke a gefen
da yake kurkusa da wuri mai tsarki kamu ɗari ne. 9 Ɗakunan da suke can ƙasa suna
da ƙofar shiga a wajen gabas in za a shiga cikinsu daga filin da yake waje.

10 A wajen kudu[*] a ta katangar filin da yake waje, kusa da filin haikali da yake
ɗaura da katangar waje, akwai ɗakuna 11 da hanya a gabansu. Waɗannan sun yi
kama da ɗakunan da suke wajen arewa; tsawonsu da fāɗinsu duk iri ɗaya ne, da irin
mafita ɗaya da kuma yadda aka shirya su. Sun yi kama da ƙofofin da suke wajen
arewa 12 haka ma ƙofofin ɗakunan a wajen kudu. Akwai ƙofa a farkon hanyar da
ta yi hannun riga da ɗayan katangar da ta miƙe wajen gabas, inda za a iya shiga
ɗakunan.

13 Sai ya ce mini, "Ɗakunan arewa da na kudu waɗanda suke fuskantar filin haikali
ɗakunan firistoci ne, inda firistocin da suke kusaci UBANGIJI za su ci hadayu mafi
tsarki. A can za su ajiye hadayu mafi tsarki, hadayu na gari, hadayu na zunubi
da hadayu na laifi, gama wuri mai tsarki ne. 14 Da zarar firistoci suka shiga wuri
mai tsarki, ba za su fita zuwa filin da yake waje ba sai sun tuɓe rigunan da suka yi
hidima da su, gama waɗannan masu tsarki ne. Za su sa waɗansu riguna kafin su
kusaci wuraren da mutane suke."

15 Da ya gama auna filin da yake cikin haikali, sai ya fitar da ni ta ƙofar gabas
ya auna dukan filin kewaye. 16 Ya auna gefen gabas da karan awo; ya samu kamu
ɗari biyar.[†,‡] 17 Ya auna gefen arewa da karan awon; ya samu kamu ɗari biyar. 18 Ya
auna gefen kudu da karan awon; ya samu kamu ɗari biyar. 19 Sa'an nan ya juya
zuwa gefen yamma ya auna shi da karan awon, ya samu kamu ɗari biya. 20 Ta haka
ya auna dukan kusurwoyi huɗu. Filin yana da katanga kewaye da shi, tsawon kamu
ɗari biyar, fāɗin kuma kamu ɗari biyar don yǎ raba wuri mai tsarki daga wuri marar
tsarki.

# 43

*Ɗaukaka ta komo haikali*

1 Sai mutumin ya kawo ni ƙofar da take fuskantar gabas, 2 sai na ga ɗaukakar Allah
na Isra'ila tana tahowa daga gabas. Muryarsa ta yi kamar rurin ruwaye masu gudu,
ƙasa kuma ta haskaka da ɗaukakarsa. 3 Wahayin da na gani ya yi kamar wahayin
da na gani sa'ad da ya zo don yǎ hallaka birnin, kamar kuma wahayin da na gani
kusa da Kogin Kebar, na kuwa fāɗi rubda ciki. 4 Ɗaukakar UBANGIJI ta shiga haikali
ta ƙofar da take fuskantar gabas. 5 Sa'an nan Ruhu ya ɗaga ni sama ya kawo ni cikin
fili na can ciki, ɗaukakar UBANGIJI kuwa ta cika haikalin.

6 Yayinda mutumin yana tsaye kusa da ni, na ji wani yana magana da ni daga cikin
haikalin. 7 Ya ce, "Ɗan mutum, wannan shi ne kursiyina da wurin tafin ƙafafuna.
A nan ne zan zauna a cikin Isra'ilawa har abada. Gidan Isra'ila ba zai ƙara ɓata
sunana mai tsarki ba, ko su ko sarakunansu, ta wurin karuwanci[*] da gumakan da
ba su da rai,[†] sarakunansu a masujadan kan tudu. 8 Sa'ad da suka sa madogarar
ƙofarsu kusa da madogarar ƙofata, da katanga kawai a tsakanina da su, sun ɓata
sunana mai tsarki ta wurin ayyukansu masu banƙyama. Saboda haka na hallaka su
cikin fushina. 9 Yanzu bari su kawar da karuwancinsu da gumakansu waɗanda ba
su da rai na sarakunansu daga gabana, zan kuwa zauna a cikinsu har abada.

---

[*] **42:10** Seftuwajin; Ibraniyanci Wajen gabas [†] **42:16** Dubi Seftuwajin na ayar 17; Ibraniyanci karan gwaji; haka ma a ayoyi 18 da 19. [‡] **42:16** Kamu ɗari biyar ya yi daidai kamar kamu 875 ko kuwa kamar mita 265; haka ma a ayoyi 17, 18 da 19. [*] **43:7** Ko kuwa zinansu ta ruhaniya; haka ma a aya 9 [†] **43:7** Ko kuwa gawawwaki; haka ma a aya 9

10 “Ɗan mutum, ka bayyana haikalin ga mutanen Isra’ila, don su ji kunya saboda
zunubansu. Bari su yi la’akari da fasalin, 11 kuma in suka ji kunyar abubuwan da suka
aikata, sai ka sanar musu fasalin haikalin da shirye-shiryensa, ƙofofinsa na shiga da
fita, dukan fasalinsa da dukan ƙa’idodinsa da dokokinsa. Ka rubuta waɗannan a
gabansu saboda su yi aminci da fasalinsa su kuma kiyaye dukan ƙa’idodinsa.
12 “Wannan ita ce dokar haikalin. Dukan filin da yake kewaye a kan dutsen, zai
zama wuri mafi tsarki. Dokar haikalin ke nan.

*Bagade*

13 “Waɗannan su ne aune-aunen bagade a tsawon kamu, wannan kamu shi ne
kamun tafin hannu. Zurfin magudanar ruwansa kamu ɗaya ne fāɗinsa kuma kamu
ɗaya, tare da da’ira kamun tafi ɗaya kewaye da gefensa. Wannan kuma shi ne tsayin
bagaden. 14 Daga lambatun da yake a ƙasa har zuwa ƙaramin mahaɗin da yake
ƙasa wanda ya kewaye bagade, tsayinsa kamu biyu ne, fāɗinsa kuma kamu guda.
Daga ƙaramin mahaɗi zuwa babban mahaɗin wanda ya kewaye bagade, zai zama
kamu huɗu, fāɗinsa kuwa kamu ɗaya. 15 Murhun bagaden kamu huɗu ne, akwai
ƙahoni guda huɗu sun miƙe sama daga murhun. 16 Murhun bagaden murabba’i ne,
tsawonsa kamu goma sha biyu, fāɗinsa kuma kamu goma sha biyu. 17 Gefen bisa
ma murabba’i ne, tsawonsa kamu goma sha huɗu fāɗinsa kuma kamu goma huɗu,
da da’ira da yake da fāɗin rabin kamu da magudanan ruwa kamu guda kewaye.
Matakan bagaden suna fuskantar gabas.”
18 Sai ya ce mini, “Ɗan mutum, ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa
waɗannan su ne za su zama ƙa’idodi don yin hadaya ta ƙonawa da yayyafawar jini
a kan bagaden sa’ad da aka gina shi. 19 Za ka ba da ɗan bijimi a matsayin hadaya ta
ƙonawa ga firistoci, waɗanda suke Lawiyawa, na iyalin Zadok, waɗanda suke zuwa
kusa don hidima a gabana, in ji UBANGIJI Mai Iko Duka. 20 Za ka ɗibi jininsa ka zuba
shi a ƙahoni huɗu na bagaden a gefen bisa da kuma kewaye da da’irar, ta haka za ka
tsarkake bagaden ka kuma yi kafara dominsa. 21 Za ka ɗauki bijimi na hadaya don
zunubi ka ƙone shi a sashen da aka shirya na haikalin a wani wuri waje da wuri mai
tsarki.
22 “A rana ta biyu za ka miƙa bunsuru marar lahani domin hadaya don zunubi, za
a kuma tsarkake bagaden yadda aka yi da bijimin. 23 Sa’ad da ka gama tsarkake shi,
sai ka miƙa ɗan bijimi da kuma rago daga cikin garke, dukansu marasa lahani. 24 Za
ka miƙa su a gaban UBANGIJI, firistoci kuma za su barbaɗe gishiri a kansu su kuma
miƙa su kamar hadaya ta ƙonawa ga UBANGIJI.
25 “Kwana bakwai za ka tanada bunsuru kullum domin hadaya don zunubi; za
ka kuma tanada ɗan bijimi da rago daga garke, dukansu marasa lahani. 26 Kwana
bakwai za su yi kafara saboda bagaden su kuma tsarkake shi; ta haka za su keɓe
shi. 27 A ƙarshen waɗannan kwanaki, daga rana ta takwas zuwa gaba, firistoci za su
miƙa hadayu na ƙonawa da hadayu na salama a kan bagade. Sa’an nan zan karɓe
ku, in ji UBANGIJI Mai Iko Duka.”

# 44

*Sarki, Lawiyawa, Firistoci*

1 Sai mutumin ya komo da ni zuwa ƙofar waje na wuri mai tsarki, wadda take
fuskantar gabas, tana kuwa a rufe. 2 UBANGIJI ya ce mini, “Wannan ƙofar za tă
kasance a rufe. Ba za a buɗe ta ba; ba wanda zai shiga ta wurinta. Za tă kasance
a rufe domin UBANGIJI, Allah na Isra’ila, ya shiga ta wurinta. 3 Sarki kansa ne kaɗai
zai zauna a hanyar shiga don yă ci a gaban UBANGIJI. Zai shiga ta hanyar shirayin
hanyar shiga yă kuma fita a wannan hanya.”

4 Sa'an nan mutumin ya kawo ni ta hanyar ƙofar arewa zuwa gaban haikali. Na
duba na kuma ga ɗaukakar Ubangiji tana cika haikalin Ubangiji, sai na fāɗi rubda
ciki.
5 Ubangiji ya ce mini, "Ɗan mutum, ka lura sosai, ka saurara sosai ka kuma mai
da hankali ga kome da na faɗa maka game da dukan ƙa'idodi game da haikalin
Ubangiji. Ka lura sosai da ƙofar shigar haikali da kuma dukan ƙofofin wuri mai
tsarki. 6 Faɗa wa 'yan tawayen gidan Isra'ila, 'Ga abin da Ubangiji Mai Iko Duka
yana cewa ayyukan banƙyamarku sun isa haka, ya gidan Isra'ila! 7 Ban da dukan
sauran ayyukanku na banƙyama, kun kawo baƙi marasa kaciya a zuciya da jiki a
wurina mai tsarki, kun kuma ƙazantar da haikalina yayinda kuke miƙa mini abinci,
kitse da kuma jini, kun kuma karya alkawarina. 8 A maimakon yin ayyukanku bisa
ga abubuwana masu tsarki, kun sa waɗansu su lura da wurina mai tsarki. 9 Ga abin
da Ubangiji Mai Iko Duka yana cewa ba baƙo marar kaciya a zuciya da jiki da zai
shiga wurina mai tsarki, kai, har ma da baƙin da suke zama a cikin Isra'ila.
10 " 'Lawiyawan da suka yi nesa da ni sa'ad da Isra'ila suka kauce da kuma waɗanda
suka karkata daga gare ni suka bi gumakansu, dole su ɗauki alhakin zunubinsu. 11 Za
su iya yin hidima a wurina mai tsarki, suna lura da ƙofofin haikali suna kuma hidima
a cikinsu; za su iya yankan hadayun ƙonawa da sadaka don mutane su kuma tsaya
a gaban mutane su yi musu hidima. 12 Amma domin sun yi musu hidima a gaban
gumakansu suka sa gidan Isra'ila ya yi zunubi, saboda haka na ɗaga hannu na rantse
cewa dole su ɗauki alhakin zunubinsu, in ji Ubangiji Mai Iko Duka. 13 Ba za su yi
kusa don su yi hidima kamar firistoci ko su zo kusa da abubuwana masu tsarki ko
hadayuna mafi tsarki ba; dole su sha kunya saboda ayyukansu na banƙyama. 14 Duk
da haka zan sa su su lura da ayyukan haikali da kuma dukan ayyukan da za a yi a
cikinsa.
15 " 'Amma firistoci, waɗanda suke Lawiyawa kuma zuriyar Zadok waɗanda suka
yi aminci ta wurin yin ayyukansu a wurina mai tsarki sa'ad da Isra'ilawa suka kauce
daga gare ni, su ne za su zo kusa don hidima a gabana; za su tsaya a gabana don
miƙa hadayun kitse da jini, in ji Ubangiji Mai Iko Duka. 16 Su ne kaɗai za su shiga
wurina mai tsarki; su ne kaɗai za su zo kusa da teburina don yin hidima a gabana
su kuma yi hidimata.
17 " 'Sa'ad da suka shiga ƙofofin fili na can ciki, dole su sa tufafin lilin; kada su sa
wani rigar da aka yi da ulu yayinda suke hidima a ƙofofin fili na can ciki da cikin
haikali. 18 Za su naɗa rawunan lilin a kawunansu, su kuma sa wandunan lilin. Kada
su sa wani abin da zai sa su yi zuffa. 19 Sa'ad da suka fita daga haikali zuwa fili
na waje inda mutane suke, sai su tuɓe rigunan da suka yi hidima da su su bar su
a tsarkakan ɗakuna, su sa waɗansu riguna, don kada su tsarkake mutane ta wurin
rigunansu.
20 " 'Ba za su aske kawunansu ko su bar gashin kansu ya yi tsayi ba, amma sai su
sausaye gashin kansu. 21 Kada firist ya sha ruwan inabi sa'ad da zai shiga fili na can
ciki. 22 Kada su auri gwauruwa ko macen da aka sāke; za su auri budurwai ne kaɗai
na Isra'ilawa ko gwaurayen firistoci. 23 Za su koyar da mutanena bambanci tsakanin
tsarki da rashin tsarki su kuma nuna musu yadda za su bambanta marar tsarki da
mai tsarki.
24 " 'A duk wani rashin jituwa, firistoci za su zama alƙalai su kuma yanke magana
bisa ga farillaina. Za su kiyaye dokokina da ƙa'idodina a dukan ƙayyadaddun
bukukkuwana, su kuma kiyaye Asabbataina da tsarki.
25 " 'Firist ba zai ƙazantar da kansa ta wurin zuwa kusa da gawa ba; amma,
in gawar mahaifinsa ko mahaifiyarsa, ko ɗansa ko 'yarsa, ko ɗan'uwansa ko
'yar'uwarsa ce, to, ba zai ƙazantar da kansa ba. 26 Bayan ya tsarkaka, dole yă jira har

kwana bakwai. [27] A ranar da ya shiga fili na can ciki na wuri mai tsarki don hidima
a wuri mai tsarki, zai miƙa hadaya don zunubi saboda kansa, in ji UBANGIJI Mai Iko
Duka.
[28] " 'Ni ne kaɗai zan zama abin gādon da firistoci za su kasance da shi. Kada ka ba
su wani mallaka a Isra'ila; zan zama mallakarsu. [29] Za su ci hadaya ta gari, hadaya
don zunubi da hadaya don laifi; da kuma kowane keɓaɓɓen abu a Isra'ila da za a ba
wa UBANGIJI zai zama nasu. [30] Mafi kyau na nunan farinku da kuma dukan kyautanku
na musamman za su zama na firistoci. Za ku ba su rabo na fari na ɓarzajjen hatsinku
saboda albarka ta kasance a gidanku. [31] Firistoci ba za su ci mushen tsuntsu ko na
dabba ba, ba kuwa za su ci waɗanda namun jeji suka kashe ba.

# 45

### *Rabon ƙasa*

[1] " 'Sa'ad da kuka rarraba ƙasar gādo, ku miƙa wa UBANGIJI rabon ƙasar ya zama
yanki mai tsarki, tsawonsa ya zama kamu 25,000 fāɗinsa kuma ya zama 20,000, dukan
ƙasar za tă zama mai tsarki. [2] Daga cikin wannan, sashe guda da yake murabba'i mai
tsawo kamu 500 zai zama don wuri mai tsarki, kamu 50 kewaye da shi zai zama fili.
[3] A cikin yanki mai tsarki, ka auna tsawo kamu 25,000 da kuma fāɗi kamu 10,000.
A cikinsa wuri mai tsarki zai kasance, Wuri Mafi Tsarki. [4] Zai zama tsattsarkan
rabo na ƙasa domin firistoci, waɗanda za su yi hidima a cikin wuri mai tsarki da
kuma waɗanda za su zo kusa don su yi hidima a gaban UBANGIJI. Zai zama wuri don
gidajensu ya kuma zama tsattsarkan wuri saboda wuri mai tsarki. [5] Wani sashi kuma
mai tsawo kamu 25,000 da fāɗi 10,000 zai zama na Lawiyawa, waɗanda suke hidima
a cikin haikali, zai zama mallakarsu don su zauna a ciki.
[6] " 'Za ka ba wa birnin fāɗin mallakarsa kamu 5,000, tsawonsa kuma 25,000, haɗe
da tsattsarkan rabo; zai kasance na gidan Isra'ila duka.
[7] " 'Sarki zai kasance da fili da ya yi iyaka da kowane gefe na yankin wuri mai
tsarki da kuma mallakar birnin. Zai miƙe ya yi wajen yamma daga gefen yamma ya
kuma yi wajen gabas daga gefen gabas, yana miƙewa a tsawo daga wajen yamma
zuwa wajen gabashin iyaka don yă yi hannun riga da rabon kabilan. [8] Wannan fili
zai zama mallakarsa a Isra'ila. Kuma sarakunana ba za su ƙara zaluntar mutanena
ba amma za su bar gidan Isra'ila ya mallaki ƙasar bisa ga kabilansu.
[9] " 'Ga abin da UBANGIJI Mai Iko na ce ku sarakunan Isra'ila, danniya da zaluncin
da kuke yi sun isa! Ku yi shari'a bisa ga gaskiya da adalci, ku bar korar mutanena,
in ji UBANGIJI Mai Iko Duka. [10] Ku yi amfani da garwan da yake daidai, efa* da yake
daidai da kuma garwa† da yake daidai. [11] Efa da garwan su kasance girmansu ɗaya,
garwan ya zama kashi ɗaya bisa goma na ganga‡ efa kuma ya zama kashi ɗaya bisa
goma na ganga; ganga fitaccen ma'auni na duka biyu. [12] Shekel zai kasance da gera
ashirin. Shekel ashirin a haɗa da shekel ashirin da biyar a haɗa da shekel goma sha
biyar zai zama mina guda.§

### *Hadayu da ranaku masu tsarki*

[13] " 'Wannan ita ce bayarwa ta musamman da za ku miƙa, kashi ɗaya bisa shida
na efa daga kowace gangan alkama da kashi ɗaya bisa shida na efa daga kowace
gangan sha'ir. [14] Sashe na man da aka ƙayyade, da aka auna da garwa, kashi ɗaya
bisa goma ne na garwa daga ganga (wanda yakan ci garwa goma, gama garwa goma
suna daidai da ganga guda). [15] A kuma ba da tunkiya daga kowane garke mai tumaki
ɗari biyu daga makiyaya da aka yi masa banruwa sosai na Isra'ila. Za a yi amfani da

* **45:10** Efa abin awo ne na busassun abubuwa. † **45:10** Garwa abin awo ne na abubuwan da suke ruwa-ruwa.
‡ **45:11** Ganga abin awo ne na busassun abubuwa. § **45:12** Wato, shekel 60; mina da aka saba amfani kan ci shekel 50.

waɗannan don hadayun gari, hadayun ƙonawa da hadayun salama don yin kafara
saboda mutane, in ji UBANGIJI Mai Iko Duka. 16 Dukan mutanen ƙasar za su yi wannan
bayarwa ta musamman saboda amfanin sarki a Isra'ila. 17 Zai zama hakkin sarki
ne ya tanada hadayu na ƙonawa, hadayu na gari da hadayu na sha a bukukkuwa,
Sabuwar Wata da Asabbatai, a duk ƙayyadaddun bukukkuwa na gidan Isra'ila. Zai
tanada hadayu don zunubi, hadayu na gari, hadayu na ƙonawa da hadayu na salama
don yin kafara saboda gidan Isra'ila.

*(Fitowa 12.1-20; Firistoci 23.33-43)*

18 " 'Ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa a farkon wata a rana ta fari za
ku ba da ɗan bijimi marar lahani a kuma tsarkake wuri mai tsarki. 19 Firist zai ɗibi
jinin hadaya don zunubi ya shafa a madogaran ƙofar haikali, a kusurwoyi huɗu na
gefen bisa na bagade da kuma a kan madogaran ƙofar shiga na fili na can ciki. 20 Za
ku yi haka kuma a rana ta bakwai ga watan domin duk wanda ya yi zunubai ba da
gangan ba ko ta wurin rashin sani; saboda haka sai ku yi kafara domin haikalin.

21 " 'A wata na fari a rana ta goma sha huɗu za ku kiyaye Bikin Ketarewa, bikin
da yakan ɗauki kwana bakwai, a lokacin ne za ku riƙa cin burodi marar yisti. 22 A
wannan rana sarki zai tanada bijimi a matsayin hadaya don zunubi domin kansa
da kuma domin dukan mutanen ƙasar. 23 Kowace rana a kwanaki bakwai na Bikin
zai tanada bijimai guda bakwai da raguna bakwai marar lahani a matsayi hadaya ta
ƙonawa ga UBANGIJI, da kuma bunsuru saboda hadaya don zunubi. 24 Zai tanada efa
na gari don kowane bijimi da kuma efa don kowane rago, tare da kwalabar mai don
kowane efa guda.

25 " 'A lokacin kwana bakwai na Bikin, waɗanda za su fara a wata na bakwai a
rana ta goma sha biyar, zai ba da abubuwan nan saboda hadayu don zunubi, hadayu
na ƙonawa, hadayu na gari da kuma mai.

# 46

1 " 'Ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa a rufe ƙofa ta fili na can cikin da
take fuskantar gabas ranaku shida na aiki, amma a ranar Asabbaci da kuma a ranar
ganin Sabuwar Wata a buɗe ta. 2 Sarki zai shiga daga waje ta shirayin hanyar shiga
yă tsaya a madogarar ƙofa. Firistoci za su miƙa hadayarsa ta ƙonawa da hadayunsa
na salama. Zai yi sujada a madogarar ƙofar hanyar shiga sa'an nan ya fita, amma ba
za a rufe ƙofar ba sai da yamma. 3 A Asabbatai da kuma a Sabuwar Wata mutanen
ƙasar za su yi sujada a gaban UBANGIJI a mashigin wannan hanyar shiga. 4 Hadaya
ta ƙonawar da sarki ya kawo wa UBANGIJI a ranar Asabbaci 'yan raguna shida ne da
rago guda, dukansu marasa lahani. 5 Hadayar garin da aka bayar tare da ragon efa
guda ne, hadayar garin da 'yan ragunan yadda ya ga dama, tare da kwalabar mai don
kowace efa. 6 A ranar Sabuwar Wata zai miƙa ɗan bijimi, 'yan raguna guda shida da
kuma rago guda, dukansu marasa lahani. 7 Zai tanada a matsayin hadaya ta gari, efa
guda tare da bijimi, efa guda tare da 'yan raguna, da kuma 'yan raguna yadda ya ga
dama, tare da kwalabar mai don kowace efa. 8 Sa'ad da sarki zai shiga, zai shiga ta
shirayin hanyar shiga, zai kuma fita ta nan.

9 " 'Sa'ad da mutanen ƙasar suka zo gaban UBANGIJI a ƙayyadaddun bukukkuwa,
duk wanda ya shiga ta ƙofar arewa don yă yi sujada sai ya fita ta ƙofar kudu; kuma
duk wanda ya shiga ta ƙofar kudu sai ya fita ta ƙofar arewa. Ba wanda zai koma ta
ƙofar da ya shiga, amma kowa zai fita a ƙofar ɗaura da wadda ya shiga. 10 Sarki zai
kasance a cikinsu, zai shiga sa'ad da suke shiga ya kuma fita sa'ad da suka fita.

11 " 'A bukukkuwa da ƙayyadaddun bukukkuwa, hadaya ta gari zai zama efa tare
da bijimi, efa da rago, da kuma 'yan raguna da ya ga dama, haɗe da kwalabar mai.
12 Sa'ad da sarki ya ba da hadaya ta yardar rai ga UBANGIJI, ko hadaya ta ƙonawa

ce ko hadayun salama ne, sai a buɗe masa ƙofar da take fuskantar gabas. Zai miƙa
hadayarsa ta ƙonawa ko hadayarsa ta salama yadda yakan yi a ranar Asabbaci. Sa'an
nan ya fita, bayan kuma ya fita, sai a rufe ƙofar.
13 " 'Kullum za ku tanada ɗan rago bana ɗaya marar lahani don hadaya ta ƙonawa
ga UBANGIJI; kowace safiya za ku tanada shi. 14 Tare da shi za ku tanada hadaya ta
gari kowace safiya, da ya haɗa da kashi ɗaya bisa shida na efa tare da kashi ɗaya
bisa uku na mai ga garin da aka cuɗa. Miƙawar wannan hadaya ta gari ga UBANGIJI
dawwammamiyar farilla ce. 15 Saboda haka za a tanada ɗan rago da hadaya ta gari
da kuma mai kowace safiya don hadaya ta ƙonawa ta kullum.
16 " 'Ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa in sarkin ya ba wa ɗaya daga
cikin 'ya'yansa kyauta daga gādonsa, zai kuwa zama na zuriyar; zai kuwa zama
mallakarsu ta wurin gādo. 17 In kuma ya ba wa ɗaya daga cikin bayinsa kyauta
daga gadonsa, bawan zai iya riƙe shi sai shekarar 'yantarwa; sa'an nan ya mayar wa
sarkin. Gādon sarki na 'ya'yansa maza ne kaɗai; na su ne. 18 Kada sarki ya ƙwace
gādon mutane, yana korinsu daga mallakarsu. Zai ba wa 'ya'yansa maza gādonsu
daga cikin mallakarsa, don kada a raba wani daga mutanena da mallakarsa.' "
19 Sa'an nan mutumin ya fitar da ni ta ƙofar shiga a gefen ƙofar zuwa tsarkakakkun
ɗakuna waɗanda suke fuskantar arewa, waɗanda suke na firistoci, ya kuma nuna
mini wani wuri daga can ƙurewar yamma. 20 Ya ce mini, "Wannan shi ne wurin da
firistoci za su dafa hadaya don laifi, da hadaya don zunubi, a nan ne kuma za su toya
hadaya ta gari, domin kada su kai su a filin da yake waje, su tsarkake mutane."
21 Sa'an nan ya kawo ni filin da yake waje ya kuma bi da ni kewaye da kusurwoyi
huɗunsa, na kuma ga kowace kusurwa na wani fili. 22 A kusurwoyi huɗu na filin
da yake waje akwai waɗansu filaye a haɗe, tsawonsu kamu arba'in fāɗinsu kuwa
kamu talatin; kowane fili a kusurwoyi huɗun nan girmansu ɗaya ne. 23 Kewaye da
cikin kowane filin huɗun nan akwai ginin dutse, da murhu da aka gina a kewaye a
ƙarƙashin ginin. 24 Sai ya ce mini, "Waɗannan su ne ɗakunan dahuwa inda masu
hidima a haikali za su dafa hadayun da jama'a."

# 47

*Kogin da ya malalo daga haikali*

1 Mutumin ya komo da ni zuwa mashigin haikalin, sai na kuwa ga ruwa yana
malalowa daga ƙarƙashin madogarar ƙofar haikalin wajen gabas (gama haikalin
yana fuskantar gabas). Ruwan yana malalowa daga ƙarƙashin gefen kudun haikalin,
kudu da bagaden. 2 Sai ya fitar da ni ta ƙofar arewa ya kewaye da ni ta waje zuwa
ƙofar da take waje mai fuskantar gabas, ruwan kuwa yana malalowa daga wajen
kudu.
3 Yayinda mutumin ya yi wajen gabas da karan awo a hannunsa, sai ya auna kamu
dubu ya kuma bi da ni ta ruwan da zurfinsa ya kama ni a idon ƙafa. 4 Ya auna
wani kamu dubu ya kuma bi da ni a ruwan da zurfinsa ya kai ni gwiwa. Ya sāke
auna kamu dubu ya kuma bi da ni a ruwan da zurfinsa kama ni a gindi. 5 Ya auna
wani kamu dubu, amma a yanzu ruwan ya zama kogin da ban iya hayewa ba, domin
ruwan ya taso ya kuma yi zurfin da ya isa a yi iyo a ciki, kogin da ba za a iya hayewa
ba. 6 Sai ya ce mini, "Dan mutum, ka ga wannan?"
Sa'an nan ya komo da ni zuwa bakin kogin. 7 Sa'ad da na iso can, sai na ga itatuwa
masu yawa a kowane gefen kogin. 8 Sai ya ce mini, "Wannan ruwa yana malalowa
zuwa yankin gabas ya kuma gangaro zuwa cikin Araba,* inda zai shiga Teku. Sa'ad
da ya shiga cikin Tekun sai ruwan a can ya zama mai daɗi. 9 Tarin halittu masu

* **47:8** Ko kuwa Kwarin Urdun

rai za su rayu a duk inda ruwan ya malalo. Za a kasance da kifi masu yawa, domin
wannan ruwa yana malalowa a can yana kuma mai da ruwan gishiri yă zama ruwa
mai daɗi; saboda haka duk inda ruwan ya malalo, kome zai rayu. [10] Masunta za su
tsaya a gaɓar; daga En Gedi zuwa En Eglayim, za a kasance da wuraren jefa abin
kamun kifi. Za a sami kifayen iri-iri, kamar kifaye Bahar Rum.† [11] Amma fadamun
da tafkunan ba za su zama masu daɗi ba; za a bar su a gishirinsu. [12] ʼYaʼyan itatuwa
na kowane iri za su yi girma a kowane gefen kogin. Ganyayensu ba su bushe ba, ba
kuwa za su fasa yin ʼyaʼya ba. Kowane wata za su ba da ʼyaʼya domin ruwa daga
wuri mai tsarki yana malalo musu. ʼYaʼyansu za su zama abinci, ganyayensu kuma
za su zama magani."

### *Iyakokin ƙasar*

[13] Ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka yana cewa, "Waɗannan su ne iyakokin da za
ku raba ƙasar gādo cikin kabilan Israʼila goma sha biyu, da rabo biyu don Yusuf.
[14] Za ku raba ta daidai a cikinsu. Gama na ɗaga hannu na rantse zan ba da ita ga
kakanninku, wannan ƙasa za tă zama gādonku.

[15] "Wannan ce za tă zama iyakar ƙasa.

"A wajen arewa za tă fara daga Bahar Rum ta hanyar Hetlon ta wuce Lebo Hamat
zuwa Zedad, [16] Berota‡ da Sibrayim (wadda take a iyaka tsakanin Damaskus da
Hamat), har zuwa Hazer-Hattikon, wadda take a iyakar Hauran. [17] Iyakar za tă
miƙe daga teku zuwa Hazar-Enon, ta iyakar Damaskus, da iyakar Hamat a arewa.
Wannan ita ce iyakar a wajen arewa.

[18] A wajen gabas iyakar za tă kama tsakanin Hauran da Damaskus, ta bi ta Urdun
tsakanin Gileyad da ƙasar Israʼila, zuwa tekun gabas har zuwa Tamar.§ Wannan
ita ce iyakar a wajen gabas.

[19] A wajen kudu za tă fara daga Tamar har zuwa ruwan Meriba Kadesh, saʼan nan
ta bi Rafin Masar zuwa Bahar Rum. Wannan ita ce iyakar a wajen kudu.

[20] A wajen yamma, Bahar Rum ne zai zama iyakar zuwa wani wuri ɗaura da Lebo*
Hamat. Wannan ita ce iyakar a wajen yamma.

[21] "Za ku rarraba wannan ƙasa a tsakaninku bisa ga kabilan Israʼila. [22] Za ku raba
ta kamar gādo wa kanku da kuma wa baƙin da suka zauna a cikinku waɗanda suke
da ʼyaʼya. Za ku ɗauka su kamar ʼyan ƙasa haifaffun Israʼilawa; za su yi gādo tare
da ku a cikin kabilan Israʼila. [23] A duk kabilar da baƙon yake zama, a can za ku ba
shi gādonsa," in ji UBANGIJI Mai Iko Duka.

# 48

### *Rarraba ƙasar*

[1] "Ga kabilan, a jere bisa ga sunayensu.

"A iyaka ta arewa, Dan zai sami rabo; zai bi hanyar Hetlon zuwa Lebo* Hamat.
Hazar-Enan da iyakar arewancin Damaskus kusa da Hamat za tă zama sashen
iyakarsa a wajen gabas zuwa wajen yamma.

[2] Asher zai sami rabo; zai yi iyaka da yankin Dan daga gabas zuwa yamma.

[3] Naftali zai sami rabo; zai yi iyaka da yankin Asher daga gabas zuwa yamma.

† **47:10** Wato, Mediterraniyan; haka ma a ayoyi 15, 19 da 20 ‡ **47:16** Dubi Seftuwajin da kuma Ezk 48.1; Ibraniyanci hanya zuwa cikin Zedad, 16 Hamat, Berota. § **47:18** Seftuwajin da Siriyak; Ibraniyanci Israʼila. Za ka auna zuwa tekun gabas. * **47:20** Ko kuwa ɗaura da ƙofar zuwa * **48:1** Ko kuwa zuwa ƙofar

4 Manasse zai sami rabo; zai yi iyaka da yankin Naftali daga gabas zuwa yamma.
5 Efraim zai sami rabo; zai yi iyaka da yankin Manasse daga gabas zuwa yamma.
6 Ruben zai sami rabo; zai yi iyaka da Efraim daga gabas zuwa yamma.
7 Yahuda zai sami rabo; zai yi iyaka da yankin Ruben daga gabas zuwa yamma.

8 “Kusa da yankin Yahuda daga gabas zuwa yamma zai zama rabon da za ku bayar
a matsayin kyauta ta musamman. Faɗinsa zai zama kamu 25,000, tsawonsa kuma zai
zama daidai da tsawon yankunan kabilu daga gabas zuwa yamma; wuri mai tsarki
zai kasance a tsakiyar wannan yanki.
9 “Tsawon rabo na musamman da za ku bayar ga UBANGIJI zai zama kamu 25,000,
fāɗinsa kuma kamu 10,000. 10 Wannan ne zai zama tsattsarkan rabo domin firistoci.
Tsawon zai zama kamu 25,000 a wajen arewa, fāɗin kuma kamu 10,000 wajen
yamma, kamu 10,000 zai zama fāɗinsa a wajen gabas, tsawonsa a wajen kudu
zai zama kamu 25,000. A tsakiyarsa ne wuri mai tsarki na UBANGIJI zai kasance.
11 Wannan zai zama na keɓaɓɓun firistoci, zuriyar Zadok, waɗanda suka yi aminci
cikin hidimata ba su kuwa karkata kamar yadda Lawiyawa suka yi sa’ad da Isra’ilawa
suka karkace ba. 12 Zai zama kyauta ta musamman a gare su daga tsattsarkan rabon
ƙasar, kusa da yankin Lawiyawa.
13 “Dab da yankin firistoci, Lawiyawa za su sami rabo mai tsawon kamu 25,000,
fāɗin kuma kamu 10,000. Tsawonsa gaba ɗaya zai zama kamu 25,000, fāɗinsa kuma
kamu 10,000. 14 Ba za su sayar da shi ko su musayar da wani sashensa ba. Wannan
shi ne mafi kyau na ƙasar ba kuma za a jinginar da ita ga wani ba, gama mai tsarki
ce ga UBANGIJI.
15 “Sauran wurin da ya rage mai fāɗin kamu 5,000 da tsawon kamu 25,000 zai
zama don amfanin kowa a birnin, don gidaje da wurin kiwo. Birnin zai kasance a
tsakiyar wurin da ya ragen nan 16 zai kuwa kasance da wannan awon, a wajen arewa
kamu 45,000, wajen kudu kamu 45,000, wajen gabas kamu 45,000, wajen kudu kuma
kamu 45,000. 17 Wurin kiwo don birnin zai zama kamu 250 a wajen arewa, kamu
250 a wajen kudu, kamu 250 a wajen gabas da kuma kamu 250 a wajen yamma.
18 Tsawon abin da ya rage a wurin, dab da tsattsarkan rabo, zai zama kamu 10,000
wajen gabas, kamu 10,000 kuma wajen yamma. Amfanin da zai bayar zai tanada
abinci don ma’aikatan birnin. 19 Masu aiki daga birnin waɗanda suka nome ta za su
fito daga dukan kabilan Isra’ila. 20 Dukan rabon zai zama murabba’i, kamu 25,000
kowane gefe. A matsayin kyauta ta musamman za ku keɓe tsattsarkan rabo, haka
ma za ku yi da mallakar birnin.
21 “Abin da ya rage a kowane gefe na wurin zai zama tsattsarkan rabo kuma
mallakar birnin za tă zama ta sarki. Zai miƙe wajen gabas daga kamu 25,000 na
tsattsarkan rabo zuwa iyakar da take wajen gabashin iyaka, da kuma a wajen yamma
kamu 25,000 zuwa iyakar da take a wajen yamma. Dukan wuraren nan da suke
hannun riga da rabon kabilan zai zama na sarki, tsattsarkan rabon tare da wuri mai
tsarkin za su kasance a tsakiyarsu. 22 Ta haka mallakar Lawiyawa da mallakar birnin
za su kasance a tsakiyar wurin da yake na sarki. Wurin da yake na sarki zai kasance
tsakanin iyakar Yahuda da iyakar Benyamin.

23 “Game da sauran kabilun kuwa,

“Benyamin zai sami rabo; zai miƙe daga wajen gabas zuwa wajen yamma.
24 Simeyon zai sami rabo; zai yi iyaka da yankin Benyamin daga gabas zuwa yamma.
25 Issakar zai sami rabo; zai yi iyaka da yankin Simeyon daga gabas zuwa yamma.

26 Zebulun zai sami rabo; zai yi iyaka da yankin Issakar daga gabas zuwa yamma.
27 Gad zai sami rabo; zai yi iyaka da yankin Zebulun daga gabas zuwa yamma.
28 Iyakar kudu ta Gad za tă miƙe kudu daga Tamar zuwa ruwan Meriba Kadesh, sa’an nan ta bi Rafin Masar zuwa Bahar Rum.†

29 “Wannan ce ƙasar da za ku raba gādo ga kabilan Isra’ila, kuma wannan ne zai zama rabonsu,” in ji UBANGIJI Mai Iko Duka.

### *Kofofin sabon birni*

30 “Waɗannan za su zama ƙofofin birnin.

“Farawa da gefen arewa, wanda yake da tsawon kamu 4,500 31 za a ba wa ƙofofin
birnin sunaye kabilan Isra’ila. Kofofi uku a gefen arewa za su zama ƙofar Ruben, ƙofar Yahuda da ƙofar Lawi.
32 A gefen gabas, wanda yake da tsawon kamu 4,500 zai kasance da ƙofofi uku, ƙofar Yusuf, ƙofar Benyamin da ƙofar Dan.
33 A gefen kudu, wanda yake da tsawon kamu 4,500, zai kasance da ƙofofi uku, ƙofar Simeyon, ƙofar Issakar da ƙofar Zebulun.
34 A gefen yamma, wanda yake da tsawon kamun 4,500, zai kasance da ƙofofi uku, ƙofar Gad, ƙofar Asher da kuma ƙofar Naftali.

35 “Duk nisan wurare kewaye da birnin zai zama kamu 18,000 ne.

“Sunan birnin kuwa daga wannan lokaci zai zama, ‘UBANGIJI yana a nan.’ ”

---

† **48:28** Wato, Mediterraniyan

# Daniyel

*Horarwar Daniyel a Babilon*

1 A Shekara ta uku ta mulki Yehohiyakim sarkin Yahuda, Nebukadnezzar sarkin
Babilon ya zo Urushalima ya kuma yi mata ƙawanya. 2 Sai Ubangiji ya bashe
Yehohiyakim sarkin Yahuda a hannunsa, tare da waɗansu kayayyakin haikalin Allah.
Ya ɗauki waɗannan kayan zuwa cikin haikalin allahnsa a Babilon* cikin ma'ajin
gidan allahnsa.
3 Sa'an nan sarkin ya umarci Ashfenaz, shugaban fadarsa yă kawo waɗansu daga
cikin Isra'ilawan da suka fito daga gidan sarauta da kuma na fitattun mutane.
4 Matasa maza waɗanda ba su da wata naƙasa kuma kyawawa, hazikai ta kowace
hanyar koyo, sanannu, masu saurin fahimtar abu, da kuma waɗanda suka cancanci
su yi aiki a fadar sarki. Zai koya musu harshen Babiloniyawa da kuma littattafansu.†
5 Sarki kuma ya sa a ba su abinci da ruwan inabi kowace rana daga cikin abincin
sarki. Za a koyar da su har shekaru uku, bayan haka kuma su shiga yin wa sarki
hidima.
6 Daga cikin waɗannan da aka zaɓa akwai waɗansu daga Yahuda, Daniyel,
Hananiya, Mishayel da kuma Azariya. 7 Sai sarkin fada ya raɗa musu sababbin
sunaye, ga Daniyel ya raɗa masa Belteshazar; ga Hananiya ya raɗa masa Shadrak;
ga Mishayel ya raɗa masa Meshak; ga Azariya kuma ya raɗa masa Abednego.
8 Amma Daniyel ya ƙudura a zuciyarsa ba zai ƙazantar da kansa da abinci da
ruwan inabin sarki ba, sai ya tambayi sarkin fada don a ba shi izinin kada yă ƙazantar
da kansa ta wannan hanya. 9 Sai Allah ya sa sarkin fada ya nuna masa tagomashi
ya kuma ƙaunaci Daniyel, 10 amma sai sarkin fada ya ce wa Daniyel, "Ina jin tsoron
ranka yă daɗe, sarkina wanda ya sa a ba ku abinci da ruwan inabi. Me zai sa yă ga
kuna ramewa fiye da sauran samari, tsaranku? Sarki zai sa a fille mini kai saboda
ku."
11 Sai Daniyel ya ce wa mai gadi wanda sarkin fada ya sa yă kula da Daniyel,
Hananiya, Mishayel da Azariya, 12 "Ina roƙonka ka gwada bayinka kwana goma.
Kada ka ba mu kome sai kayan lambu mu ci da kuma baƙin ruwa mu sha. 13 Sa'an
nan sai ka dubi fuskokinmu da na sauran samarin da suke ci daga abincin sarki;
sa'an nan ka yi da bayinka bisa ga abin da ka gani." 14 Sai ya amince da haka ya
kuma gwada su har kwana goma.
15 A ƙarshen kwana goma sai aka ga fuskokinsu suna sheƙi, sun kuma yi ƙiba fiye
da samarin da suke cin abinci irin na sarki. 16 Sai mai gadinsu ya janye abinci da
ruwan inabi irin na sarki, ya ci gaba da ba su kayan lambu.
17 Ga samarin nan guda huɗu Allah ya ba su sani da ganewar dukan irin littattafai
da kuma koyarwa. Daniyel kuma ya iya gane wahayi da kowane irin mafarki.
18 A ƙarshen lokacin da sarki ya sa da za a kawo su ciki, sai sarkin fada ya gabatar
da su ga Nebukadnezzar. 19 Sarki kuwa ya yi magana da su, sai ya gano cewa babu
wani kamar Daniyel, Hananiya, Mishayel da kuma Azariya; don haka sai suka shiga yi
wa sarki hidima. 20 A dukan al'amuran hikima da na fahimta wanda sarki ya tambaye
su, ya tarar sun fi dukan masu sihiri da bokaye waɗanda suke cikin mulkinsa sau
goma.
21 Daniyel kuwa ya kasance a nan har shekara ta farko ta mulkin sarki Sairus.

* **1:2** Shinar na Ibraniyanci † **1:4** Ko kuwa Kaldiyawa

# 2

*Mafarkin Nebukadnezzar*

1 A shekara ta biyu ta mulkinsa, Nebukadnezzar ya yi mafarkai; hankalinsa ya tashi
har ya kāsa barci. 2 Sai sarki ya sa aka tattara masa masu sihiri da masu dabo da
bokaye da masanan taurari* domin su faɗi abin da ya yi mafarki a kai. Da suka shigo
suka tsaya a gaban sarki, 3 sai ya ce musu, "Na yi mafarkin da ya dame ni kuma ina
so in san me yake nufi."†
4 Sai masanan taurarin suka amsa wa sarki da Arameyanci‡ "Ran sarki yă daɗe!
Ka faɗa wa bayinka mafarkin, mu kuma sai mu fassara."
5 Sai sarki ya amsa wa masanan taurarin ya ce, "Na mance da abin, idan ba ku
tuno mini mafarkin, duk da fassararsa ba, to, za a daddatse ku gunduwa-gunduwa, a
mai da gidajenku juji. 6 Amma in har kuka faɗa mini mafarkina kuka kuma bayyana
fassararsa, za ku sami lada mai girma. Saboda haka ku faɗa mini mafarkin da kuma
fassararsa."
7 Sai suka sāke amsa masa suka ce, "Ran sarki yă daɗe, faɗa wa bayinka mafarkin,
mu kuma za mu fassara shi."
8 Sai sarki ya amsa ya ce, "Na gane cewa kuna ƙoƙari ku ɓata lokaci ne kawai
domin ku ga na manta da abin. 9 In ba ku faɗa mini mafarkin ba, akwai hukunci
guda ɗaya kurum dominku. Kun haɗa baki domin ku faɗa mini munanan al'amura
domin ku ruɗe ni har lokaci yă wuce. Sai ku faɗa mini mafarkin, ta haka kuwa zan
sani za ku iya yi mini fassararsa."
10 Sai masanan taurarin suka amsa wa sarki suka ce, "Babu wani mutum a duniyan
nan da zai iya yin abin da sarki yake nema! Babu wani sarki mai daraja da girma
wanda ya taɓa yin irin wannan tambaya ga masu sihiri ko masu dabo ko masanan
taurari. 11 Abin da sarki yake nema yana da wuya matuƙa. Babu wani da zai iya
bayyana wannan ga sarki sai dai alloli; kuma ba su zama tare da 'yan adam."
12 Wannan ya sa sarki ya fusata ƙwarai, ya ba da umarni a tafi da dukan masu
hikima na Babilon a kashe su. 13 Sai aka ba da dokar da za a kashe masu hikima,
sa'an nan aka aika mutane su je su nemo Daniyel da abokansa domin a kashe su.
14 Sa'ad da Ariyok, shugaban ƙungiyar matsaran sarki, ya fita domin yă kashe
masu hikima na Babilon, sai Daniyel ya yi masa magana cikin hikima da dabara.
15 Ya tambayi mai tsaro na sarki, "Me ya sa sarki ya fitar da wannan doka haka da
fushi?" Sai Ariyok ya yi wa Daniyel bayanin batun. 16 Da jin haka sai Daniyel ya
tafi wurin sarki ya nemi ƙarin lokaci, domin yă bayyana wa sarki mafarkin da kuma
fassararsa.
17 Sa'an nan Daniyel ya komo gida ya kuma sanar wa abokansa Hananiya, Mishayel
da Azariya, batun nan duka. 18 Ya roƙe su su roƙi jinƙan Allah na sama domin
wannan mafarki, saboda kada a kashe shi da abokansa tare da sauran masu hikima
na Babilon. 19 A wannan dare sai aka bayyana wa Daniyel mafarkin cikin wahayi.
Daniyel kuwa ya ɗaukaka Allah na sama. 20 Ya ce,
"Yabo ya tabbata ga sunan Allah har abada abadin;
hikima da iko nasa ne.
21 Yana sāke lokuta,
yana tuɓe sarakuna yana kuma naɗa waɗansu.
Yana ba da hikima ga masu hikima
kuma ilimi ga masu basira.
22 Yakan bayyana zurfafa da ɓoyayyun abubuwa;
ya san abin da yake cikin dare,

* **2:2** ko na Kaldiyawa; da wanda har yanzu yake a aya ta 4, 5 da 10 † **2:3** ko me wannan ya nuna ‡ **2:4** daga ayoyin nan zuwa sura 7 da Arameyanci ne.

haske kuwa yana zaune tare da shi.
23 Na gode maka ina yabonka, Allah na kakannina.
Kai ka san hikima da iko,
ka sanar da ni abin da muka tambaye ka, ka kuma sanar da mu mafarkin sarki."

*Daniyel ya fassara mafarkin*

24 Sai Daniyel ya tafi wurin Ariyok, wanda sarki ya sa yǎ kashe masu hikiman
Babilon, ya kuma ce masa, "Kada ka kashe masu hikiman Babilon ka kai ni wurin
sarki, ni kuma zan fassara masa mafarkinsa."
25 Sai Ariyok ya kai Daniyel wurin sarki nan take ya ce masa, "Na gano wani mutum
daga cikin kamammun kabilar Yahuda wanda zai faɗa wa sarki abin da mafarkin
yake nufi."
26 Sarki ya tambayi Daniyel (wanda ake kira Belteshazar), za ka iya faɗa mini
mafarkin da na yi ka kuma fassara shi?
27 Daniyel ya amsa, "Babu wani mai hikima, ko mai sihiri, ko mai dabo ko mai
duban da zai iya warware wa sarki wannan matsala da ta dame shi, 28 amma akwai
Allahn da yake a sama wanda yake bayyana asirai, ya nuna wa sarki Nebukadnezzar
abin da zai faru a kwanaki masu zuwa. Mafarkinka da wahayin da ya wuce cikin
tunaninka a sa'ad da kake kwance a gadonka su ne,
29 "A sa'ad da kake kwance, ya sarki, tunaninka ya ga al'amuran da suke zuwa,
kuma shi mai bayyana al'amuran ya bayyana maka asiran abubuwan da za su faru.
30 Amma ba a bayyana mini wannan asiri saboda ina da wata hikima fiye da sauran
mutane ba, sai dai domin a sanar wa sarki da fassarar, ka kuma san tunanin da ya
shiga zuciyarka.
31 "Ya sarki, ka ga wata babbar siffa, mai girma, siffa ce mai haske, abar bantsoro
tana tsaye a gabanka. 32 An yi kan wannan siffa da zinariya zalla, ƙirjinta da kuma
hannuwanta an yi su da azurfa, cikinta da kuma cinyarta da tagulla ne. 33 An yi
ƙafafun da ƙarfe, tafin ƙafafunta kuma an yi rabi da ƙarfe rabi kuma da yumɓu.
34 A lokacin da kake dubawa, sai aka yanko wani dutse, amma ba da hannun mutum
ba. Ya fāɗa a kan ƙafafun siffar na ƙarfen da aka haɗa da yumɓu aka kuma ragargaje
su. 35 Sai ƙarfen da yambun da tagulla da azurfan da kuma zinariyan suka ragargaje
a lokaci ɗaya ya zama kamar ƙaiƙayi a masussuka a lokacin kaka. Sai iska ta kwashe
su ta tafi, har ba a iya ganin ko alamarsu. Amma dutsen da ya fāɗo a siffar ya girke
ya zama tsauni ya kuma cika dukan duniya.
36 "Wannan shi ne mafarkin, yanzu kuma za mu fassara ta wa sarki. 37 Ya, sarki,
kai ne sarkin sarakuna. Allah na sama ya ba ka iko da girma da suna; 38 a cikin
hannunka ya sanya ɗan adam, da namun jeji da tsuntsayen sama. A duk inda suke
zaune, ya maishe ka ka yi mulki a bisansu kai ne kan zinariyan nan na siffar.
39 "A bayanka, za a yi wani mulki, wanda bai kai naka ba. A gaba kuma, za a yi
mulki na uku wanda yake na tagulla, zai yi mulkin dukan duniya. 40 A ƙarshe, za
a yi mulki na huɗu, mai ƙarfi kamar ƙarfe, Da yake baƙin ƙarfe yakan kakkarya,
ya ragargaje abubuwa, haka nan wannan mulki zai ragargaje sauran mulkoki 41 Ka
kuma ga an yi ƙafafun da yatsotsin da baƙin ƙarfe gauraye da yumɓu, wato, mulkin
zai rabu, amma zai kasance da ƙarfi kamar na baƙin ƙarfe da yake gauraye da yumɓu.
42 Kamar yadda yatsotsin rabi na ƙarfe rabi kuma na yumɓu ne, haka wannan mulki
zai zama rabi mai ƙarfi rabi kuma marar ƙarfi. 43 Kamar dai yadda ka ga ƙarfen
ya gauraye da yumɓu, haka mutanen za su zama a gauraye amma ba za su haɗu da
juna ba, kamar yadda baƙin ƙarfe da yumɓu ba su haɗuwa.
44 "A lokacin mulkin waɗannan sarakunan, Allah na sama zai kafa mulki da ba zai
taɓa rushewa ba, ba kuma za a ba ma waɗansu mutane ba. Zai ragargaje waɗannan
mulkokin da kuma kawo su ga ƙarshe, amma shi wannan mulki zai dawwama har

abada. 45 Wannan shi ne ma'anar wannan wahayin da ka gani na dutsen da aka
yanko daga jikin tsaunin, amma ba da hannun ɗan adam ba, dutsen da ya ragargaza
ƙarfen, da tagullar, da yumɓun da azurfar da kuma zinariyar.

"Allah mai girma ya nuna wa sarki abin da zai faru nan gaba. Mafarkin gaskiya
ne, fassararsa kuma abin dogara ne."

46 Sai sarki Nebukadnezzar ya fāɗi da fuskarsa har ƙasa a gaban Daniyel domin ya
girmama shi ya kuma umarta a miƙa hadaya da kuma hadayar ƙonawa ta turare ga
Daniyel. 47 Sarki ya kuma ce wa Daniyel, "Tabbatacce Allahnka shi ne Allahn alloli da
kuma Sarkin sarakuna da mai bayyana asirai, gama ka iya bayyana wannan asiri."

48 Sai sarki ya ɗora Daniyel a babban matsayi ya kuma sanya shi mai mulki a
kan dukan yankin ƙasar Babilon; ya kuma ɗora shi yă zama mai kula da duk masu
hikima. 49 Bugu da ƙari, bisa ga bukatar Daniyel sai sarki yă naɗa Shadrak da Meshak
da Abednego su zama masu kula da harkokin lardin Babilon, amma Daniyel kuma
ya tsaya a fadar sarki.

# 3

*Siffar zinariya da tanderun wuta*

1 Sarki Nebukadnezzar ya yi gunkin zinariya, tsawonsa kamu tasa'in, fāɗinsa
kuma kamu* tara ne, ya kafa shi a filin Dura a yankin Babilon. 2 Sa'an nan ya
aika a kira hakimai da wakilai da gwamnoni da mashawarta, da ma'aji, da alƙalai,
da marubutan kotu, da dukan sauran ma'aikatan yankunan, suka hallara domin
a rusuna wa wannan siffar da ya kafa. 3 Saboda haka sai hakimai, da wakilai da
gwamnoni, mashawarta da ma'aji da alƙalai, da marubutan alƙalai, da kuma dukan
ma'aikatan yankunan suka tattaru domin kaddamar da siffar da Nebukadnezzar ya
kafa, suka kuma tsaya a gabansa.

4 Sai mai shela ya daga murya da ƙarfi ya ce, "Wannan shi ne abin da aka umarce
ku ku yi, ya ku mutane da al'umma da kowane yare. 5 Da zarar kuka ji karar ƙaho,
da sarewa, da garaya da goge da molo da algaita da kowane irin kaɗe-kaɗe da bushe-
bushe ku rusuna ku yi sujada ga wannan gunkin da sarki Nebukadnezzar ya kafa.
6 Duk wanda bai rusuna ya yi sujada ba, nan take za a jefa shi a cikin tendarun wuta."

7 Saboda haka, da zarar suka ji karar ƙaho, da sarewa, garaya da goge da kowane
irin kaɗe-kaɗe da bushe-bushe da kowane irin kaɗe-kaɗe kowane mutum da ko wace
al'umma da kowane irin yare suka sunkuya suka yi sujada ga wannan siffa ta zinariya
da sarki Nebukadnezzar ya kafa.

8 A wannan lokaci sai waɗansu masanan taurari† suka zo gaba suka yi karar
Yahudawa. 9 Suka ce wa sarki Nebukadnezzar, "Ran sarki yă daɗe, 10 Ya sarki, ka
fitar da doka, cewa duk wanda ya ji karar ƙaho, da sarewa, da garayu da goge, da
molo da algaita da kowane irin kayan kaɗe-kaɗe da bushe-bushe sai yă rusuna yă yi
sujada ga siffar zinariya, 11 kuma cewa duk wanda bai rusuna ya yi sujadar ba za a
jefa shi cikin tanderun wuta. 12 Amma sai ga waɗansu Yahudawa waɗanda ka ɗora
su a kan harkokin yankin Babilon, wato, Shadrak, Meshak da Abednego waɗanda ba
su kula da umarninka ba, ya sarki. Ba su bauta wa allolin ba balle su yi sujada ga
gunkin zinariya da ka kafa."

13 Cikin fushi da hasala, Nebukadnezzar ya aika a kira Shadrak, Meshak da
Abednego. Aka kawo waɗannan mutane a gaban sarki, 14 sai Nebukadnezzar ya
ce musu, "Gaskiya ne Shadrak, Meshak da Abednego, cewa kun ƙi ku bauta wa alloli
kuka kuma ƙi yi sujada ga gunkin da na kafa? 15 Yanzu sa'ad da kuka ji karar ƙaho, da

* **3:1** da Arameyanci yana nufin tsawonsa kamu sittin ne fāɗinsa kamu shida ne (wato, wajen taki 27, tsawonsa taki 2.7 fāɗinsa) † **3:8** Ko kuwa Kaldiyawa

sarewa, da garaya, da goge, da molo da algaita da kowane irin kaɗe-kaɗe da bushe-
bushe, in kuna a shirye ku rusuna ƙasa ku yi wa wannan gunkin da na yi sujada, to,
da kyau. Amma in ba ku yi sujada ba, za a je fa ku yanzu a cikin tanderun wutar
nan. In ga kowane ne allahn nan da zai kuɓutar da ku daga hannuna?"

16 Sai Shadrak, Meshak da Abednego suka amsa wa sarki suka ce, "Ya Nebukadnez-
zar, ba mu bukata mu kāre kanmu a gabanka a kan wannan batu. 17 In an jefa mu
cikin tanderun wutar nan, Allahn da muke bauta wa zai iya cetonmu daga ita, kuma
ya sarki, zai cece mu daga hannunka. 18 Amma ko da bai cece mu ba, muna so ka
sani, ya sarki; cewa ba za mu bauta wa allolinka ba ko kuma mu yi sujada ga gunkin
zinariyar da ka kafa ba."

19 Sai Nebukadnezzar ya husata da Shadrak, Meshak da Abednego, sai al'amuransa
a kansu ya canja. Sai ya umarta a ƙara zuga wutar har sau bakwai domin tă yi
zafi fiye da yadda take a dā. 20 Kuma ya umarci waɗansu ƙarfafan sojoji a cikin
rundunarsa su daure Shadrak, Meshak da Abednego su jefa su cikin tanderun wutar.
21 Waɗannan mutanen suna sanye da riguna, da wanduna, da rawani da waɗansu
kayan sawa, aka daure su, aka jefa su cikin tanderun wuta. 22 Sarki ya ba da umarnin
da gaggawa kuma wutar ta yi zafi ƙwarai har harshen wutar ya kashe sojojin nan da
suka ɗauki Shadrak, Meshak da Abednego, 23 waɗannan mutane uku kuma a daure,
suka fāɗa cikin tanderun wutar.

24 Sai Sarki Nebukadnezzar ya miƙe tsaye, cike da mamaki ya tambayi
mashawartansa, "Shin ba mutum uku ba ne muka daure muka jefa cikin wutar?"

Suka amsa, "Tabbatacce haka yake ya sarki."

25 Sai ya ce, "Ku duba ina ganin mutum huɗu suna tafiya suna yawo a cikin wutar,
a sake kuma babu abin da ya same su, na huɗun sai ka ce ɗan alloli."

26 Sai Nebukadnezzar ya matsa kusa da ƙofar tanderun wutar ya yi kira da ƙarfi,
"Shedrak, Meshak da Abednego, bayin Allah Mafi Ɗaukaka ku fito! Ku zo nan!"

Sai Shadrak, Meshak da Abednego suka fita daga cikin wutar, 27 Sa'an nan hakimai,
da wakilai, da gwamnoni da masu ba wa sarki shawara suka kewaya su. Suka ga
wutar ba tă yi musu wani lahani a jikinsu ba, babu ko gashin kansu da ya ƙuna; ko
warin wuta ma ba su yi ba.

28 Sa'an nan Nebukadnezzar ya ce, "Yabo ya tabbata ga Allahn Shadrak, Meshak
da Abednego wanda ya aiko da mala'ikansa ya ceci bayinsa da suka dogara matuƙa
a gare shi, suka ki bin umarnin sarki kuma su na a shirye domin su ba da ransu
da suka ƙi bauta ko su yi sujada ga wani allah sai dai Allahnsu. 29 Domin haka ina
ba da doka cewa duk mutane da kowace al'umma ko kowane yaren da ya ce wani
abu mummuna a kan Allahn Shadrak, Meshak da Abednego za a yanka shi gunduwa-
gunduwa kuma gidansu zai zama wurin zuba shara, domin babu wani allahn da zai
iya ceto ta irin wannan hanya."

30 Sa'an nan sarki ya ƙara wa su Shadrak, Meshak da Abednego girma a yankin
Babilon.

# 4

*Nebukadnezzar ya yi mafarkin itace*

1 Daga sarki Nebukadnezzar.

Zuwa ga mutane da al'ummai da kuma kowane yare, da suke zama a duniya.

Salama mai yawa ta tabbata a gare ku!

2 Ina murna in shaida muku game da alamu da al'ajabai waɗanda Allah Mafi
Ɗaukaka ya yi ta wurina.

3 Alamunsa da girma suke,
ayyukansa da girma suke!

Mulkinsa mulki ne na har abada;
saurautarsa kuma za tă dawwama daga zamani zuwa zamani.
4 Ni, Nebukadnezzar, ina zaune a gidana cikin fadata, ina jin daɗi ina bunkasa.
5 Na yi mafarkin da ya ba ni tsoro. A sa'ad da nake kwance a gadona, siffofi da
wahayoyi da suka bi ta cikin tunanina sun firgita ni. 6 Don haka na ba da umarni a
tattaro dukan masu hikima na Babilon su bayyana a gabana domin su fassara mini
mafarkin. 7 Sa'ad da masu sihiri, da masu dabo, da masanan taurari* da masu
duba suka zo, na faɗa musu mafarkin, amma ba su iya fassarta mini mafarkin ba.
8 A ƙarshe, sai Daniyel ya zo gabana na kuma faɗa masa mafarkin. (Ana ce da shi
Belteshazar, wanda aka ba shi sunan allahna kuma ruhun alloli masu tsarki suna
a bisansa.)
9 Na ce, "Belteshazar, shugaban masu sihiri, na san ruhun alloli suna a kanka,
babu wani asirin da zai fi ƙarfin ganewarka. Ga dai mafarkin da na yi, sai ka
fassara mini. 10 Waɗannan su ne wahayin da na gani a lokacin da nake kwance a
gadona, na duba, a gabana kuwa ga wani itace a kafe a tsakiyar duniya, yana da
tsawo ƙwarai. 11 Itacen ya yi girma ya kuma yi ƙarfi, har tsayinsa ya taɓa sarari
sama; ana iya ganinsa a ko'ina a duniya. 12 Ganyayensa suna da kyau, yana da
'ya'ya jingim, abinci kuma domin kowa da kowa. A ƙarƙashinsa namun jeji suke
samun wurin hutawa, kuma tsuntsayen sama suna zaune a bisa rassansa; daga
cikinsa kowace halitta take cin abinci.
13 "A cikin wahayin da gani sa'ad da nake kwance a kan gadona, Na duba, a
gabana kuwa ga wani ɗan saƙo,† mai tsarki, yana saukowa daga sama. 14 Sai
ya yi kira da babbar murya ya ce, 'A sare itacen a kuma yayyanka rassansa; a
karkaɗe ganyensa a kuma warwatsar da 'ya'yansa. Bari dabbobi su tashi daga
ƙarƙashinsa da kuma tsuntsayen da suke a rassansa. 15 Amma a bar kututturen
da kuma saiwoyinsa, a daure shi da ƙarfe da kuma tagulla, a bar shi a cikin ƙasa,
a cikin ciyayin filaye.
" 'Bari yă jiƙu da raɓar, bari yă zauna cikin dabbobi tare da tsire-tsiren duniya.
16 Bari a canja tunaninsa irin na mutane a ba shi tunani irin na dabbobi, har sau
bakwai‡ su wuce a kansa.
17 " 'An sanar da wannan matsayi ne ta bakin 'yan saƙo, masu tsarki ne kuwa
suka sanar da hukuncin, domin masu rai su sani Mafi Ɗaukaka ne mai iko duka
a bisa kowane mulkin mutane, yakan kuma ba wa duk wanda ya ga dama, yakan
sanya talaka yă zama sarki.'
18 "Wannan shi ne mafarkin da ni, Nebukadnezzar, na yi. Yanzu Belteshazar, sai
ka faɗa mini abin da yake nufi, domin babu wani a cikin masu hikima a mulkina
da ya iya fassara mini shi. Amma za ka iya, domin ruhun alloli masu tsarki yana
a bisanka."

### *Daniyel Ya Fassara Mafarkin*

19 Sai Daniyel (wanda ake kira Belteshazar) ya tsaya zugum na ɗan lokaci,
tunaninsa ya ba shi tsoro. Saboda haka sarki ya ce, "Belteshazar, kada ka bar
mafarkin ko ma'anarsa ta tayar maka da hankali."
Belteshazar ya amsa ya ce, "Ranka yă daɗe, in dai har mafarkin zai tsaya a
kan abokan gābanka da ma'anarsa kuma ta faɗa kan maƙiyan! 20 Itacen da ka
gani; wanda ya yi girma da ƙarfe, da tsayinsa ya taɓa sararin sama, wanda ana
ganinsa ko'ina a duniya, 21 wanda ganyayensa masu kyau ne yana da 'ya'yan itace
da yawa, wanda yake ba da abinci ga duka, yana ba da wurin hutu ga namun jeji,
kuma rassansa suna ɗauke da sheƙar tsuntsayen sama. 22 Ya sarki kai ne itacen

* **4:7** Ko kuwa Kaldiyawa † **4:13** Ko kuwa mai tsaro; za a kuma iya samu a aya 17 da 23 ‡ **4:16** Ko kuwa shekaru bakwai; kamar yadda yake a aya 23, 25 da 32

nan! Ka yi girma da ƙarfi; girmanka kuma ta kai har sama, mulkinka kuma ya kai ko'ina a duniya.
23 "Ya sarki ka ga ɗan saƙon mai tsarkin nan, yana saukowa daga sama yana
cewa, 'A sare itacen a hallaka shi, amma a bar kututturensa daure da ƙarfe da tagulla, a bar shi can a ɗanyar ciyawar filaye, ya jiƙe da raɓa, ya zauna tare da namun jeji har shekara bakwai.'
24 "Ga fassarar, ya sarki, wannan ita ce doka wadda Mafi Ɗaukaka ya bayar a kan
ranka yă daɗe, sarkina. 25 Za a kore ka daga cikin mutane, za ka kuma zauna cikin
namun jeji; za ka ci ciyawa kamar shanu, za ka jiƙe da raɓa har shekara bakwai cif sa'an nan za ka sani cewa Mafi Ɗaukaka ne mai iko duka a kan dukan mulkoki
a duniya, yake kuma ba da mulki ga duk wanda ya ga dama. 26 Umarni na barin
kututturen itacen da saiwoyinsa yana nufin cewa za a maido maka da mulkinka
a lokacin da ka gane cewa Mai sama ne yake mulki. 27 Saboda haka, ya sarki, ina
roƙonka ka karɓi shawarar da zan ba ka; ka furta zunubanka ta wurin yin abin da yake daidai. Ka bar muguntarka, ka aikata alheri ga waɗanda ake wulaƙantawa, wataƙila za a ƙara tsawon kwanakinka da salama."

## *Mafarkin Ya Cika*

28 Duk wannan kuwa ya faru da sarki Nebukadnezzar. 29 Bayan wata goma sha
biyu, a sa'ad da sarki yake takawa a bisan saman ɗakin fadar Babilon, 30 sai ya ce,
"Ba wannan ita ce Babilon babba da na gina domin wurin zaman sarautar Babilon, da ikona kuma domin ɗaukakar darajata ba?"
31 Tun kalmomin suna cikin bakinsa sai ya ji murya daga sama tana cewa,
"Wannan shi ne abin da aka zartar a kanka, Sarki Nebukadnezzar. An karɓe ikon
mulkinka. 32 Za a kore ka daga cikin mutane za ka kuma yi rayuwa tare da namun
jeji. Za ka ci ciyawa kamar sa har shekara bakwai cif, sa'an nan za ka gane Mafi Ɗaukaka ne mai iko duka a kan dukan mulkoki a duniya, yake kuma ba da mulki ga duk wanda ya ga dama."
33 Nan da nan abin da aka faɗa a kan Nebukadnezzar tabbatarsa ya cika. Aka
kore shi daga cikin mutane ya kuma shiga cin ciyawa kamar shanu. Jikinsa ya jiƙe da raɓa, har gashinsa ya yi tsawo kamar fikafikan gaggafa, kumbarsa kuma suka yi tsawo kamar na tsuntsu.

34 A ƙarshen waɗannan kwanaki, ni, Nebukadnezzar, na ɗaga idanuna sama, sai
hankalina ya komo mini. Na kuwa yabi Maɗaukaki, na girmama shi, na ɗaukaka shi wanda yake rayayye har abada.

Mulkinsa dawwammamen mulki ne;
saurautarsa ta dawwama daga zamani zuwa zamani.
35 Dukan mutanen duniya
ba a bakin kome suke ba.
Yakan yi abin da ya gamshe shi
da ikokin sama
da kuma na mutanen duniya.
Babu mai hana shi
ko yă ce masa; "Me ka yi?"

36 A lokacin nan hankalina ya komo mini, sai aka mayar mini da masarautata mai
daraja, da martabata, da girmana. 'Yan majalisata da fadawana suka nemo ni. Aka
maido ni kan gadon sarautata da daraja fiye da ta dā. 37 Yanzu ni, Nebukadnezzar,
ina yabon Sarkin sama, ina waƙa ina kuma darjanta shi, saboda dukan abin da ya yi mini, mai kyau ne kuma dukan hanyoyinsa gaskiya ne. Kuma duk masu tafiya da girman kai zai ƙasƙantar da su.

# 5

*Rubutu a kan bango*

1 Sarki Belshazar ya yi babban biki domin dubban hakimansa ya kuma sha ruwan
inabi tare da su. 2 Yayinda Belshazar yake shan ruwan inabi, sai ya umarta a
kawo zinariya da azurfan da Nebukadnezzar mahaifinsa* ya kwaso daga haikali
a Urushalima, saboda sarki da hakimansa, da matansa da ƙwarƙwaransa su sha
da su. 3 Sai suka kawo kayan zinariyan nan da aka kwaso daga haikalin Allah a
Urushalima, sarki kuwa da hakimansa, da matansa, da ƙwarƙwaransa suka yi ta sha
da su. 4 Yayinda suke shan ruwan inabin, sai suka yabi allolin zinariya da azurfa, da
na tagulla, da na ƙarfe, da na itace da kuma na dutse.
5 Nan da nan sai ga yatsotsin hannun mutum sun bayyana, suna yin rubutu a kan
shafen bangon, kusa da wurin da ake ajiye fitilar fadar sarki. Sarki kuwa yana ganin
hannun yayinda yake rubutu. 6 Sai fuskarsa ta ruɗe, ya kuma ji tsoro ƙwarai har
gwiwoyinsa suka yi ta bugun juna, ƙafafunsa kuma suka rasa ƙarfi.
7 Sai sarki ya kira masu dabo, masanan taurari† da masu duba, a kawo su, ya kuma
ce wa masu hikima na Babilon, "Duk wanda ya karanta wannan rubutu ya kuma
faɗa mini abin da yake nufi, za a sa masa rigar shunayya, a kuma sa masa sarƙar
zinariya a wuyansa, zai zama na uku a cikin masu mulkin ƙasar."
8 Sa'an nan sai dukan masu hikima suka zo ciki, amma ba su iya karanta rubutun
ba ko su faɗa wa sarki abin da yake nufi. 9 Saboda haka Sarki Belshazar ya firgita
ƙwarai kuma fuskarsa ta ƙara ruɗewa. Hakimansa kuma suka rikice.
10 Sai sarauniya,‡ da jin muryoyi na sarki da na hakimansa, ta shiga babban
ɗakin liyafar. Ta ce, "Ya sarki, ranka yǎ daɗe! Kada ka firgita! Kada fuskarka
ta ruɗe! 11 Akwai wani mutum a masarautarka wanda yake da ruhun alloli masu
tsarki a cikinsa. A zamanin mahaifinka an gane cewa yana da basira da hazaka da
hikima kamar na alloli. Sarki Nebukadnezzar mahaifinka, mahaifinka sarki, na ce,
ya naɗa shugaban masu dabo, da masu sihiri, masanan taurari da kuma masu duba.
12 Wannan mutum Daniyel, wanda sarki ya kira Belteshazar, an gane yana da ruhu
nagari, da ilimi, da ganewa don yin fassarar mafarkai, da bayyana ma'anar kacici-
kacici, da warware al'amura masu wuya. Ka kira Daniyel shi kuwa zai faɗa maka
abin da rubutun nan yake nufi."
13 Saboda haka aka kawo Daniyel a gaban sarki, sai sarki ya ce masa, "Kai ne
Daniyel ɗin nan, ɗaya daga cikin kamammu waɗanda mahaifina sarki ya kawo daga
Yahuda? 14 Na sami labari cewa kana da ruhun alloli a cikinka da kuma basira, da
hazaka da kuma fitacciyar hikima. 15 An kawo masu hikima da masu dabo a gabana
domin su karanta wannan rubutu su kuma faɗa mini abin da yake nufi, amma ba
su iya ba. 16 Na sami labari cewa kana iya ba da fassara da kuma warware matsaloli
masu wuya. In har ka iya karanta wannan rubutun ka kuma faɗa mini abin da yake
nufi, za a sa maka riga shunayya, a kuma sa sarƙar zinariya a wuyanka. Za ka zama
na uku a cikin masu mulkin ƙasar."
17 Sai Daniyel ya amsa wa sarki ya ce, "Za ka iya ajiye kyautar wa kanka ko kuma
ka ba wa wani. Duk da haka, zan karanta wa sarki rubutun, in kuma faɗa abin da
yake nufi.
18 "Ya sarki, Allah Mafi Ɗaukaka ya ba mahaifinka Nebukadnezzar sarauta, da
girma, da ɗaukaka, da martaba. 19 Saboda irin matsayin da ya ba shi, dukan mutane
da al'ummai da kuma dukan harsuna suka ji tsoronsa suka yi rawar jiki a gabansa.
Bisa ga ganin damarsa yakan kashe wani, ya bar wani da rai, haka kuma yakan
ɗaukaka wani, ya ƙasƙantar da wani. 20 Amma da lokacin da zuciyarsa ta cika da

* 5:2 Ko kakansa; ko wanda ya gāji sarauta daga gare shi; haka kuma a ayoyi 11, 13, da 18 † 5:7 Ko kuwa Kaldiyawa, haka ma a aya 11 ‡ 5:10 Ko kuwa mahaifiyar sarauniya

girman kai ta kuma taurare, sai aka kore shi daga gadon sarautarsa, aka raba shi
kuma da darajarsa. 21 Aka kore shi daga cikin mutane aka kuma ba shi tunani irin
na dabba; ya yi zama tare da jakunan jeji, ya kuma ci ciyawa kamar shanu; jikinsa
kuma ya jiƙe da raɓa, har zuwa lokacin da ya gane, ashe, Allah Maɗaukaki ne mai
iko duka a kan dukan mulkoki a duniya, yake kuma ba da mulki ga duk wanda ya
ga dama.

22 "Amma kai ɗansa,§ Ya Belshazar, ba ka ƙasƙantar da kanka ba, ko da yake ka
san wannan duka. 23 A maimakon, sai ka nuna wa Ubangiji na sama girman kai. Ka
sa aka kawo maka su kwaf na zinariya daga haikalinsa, da kai da hakimanka, da
matanka da ƙwarƙwaranka kuka sha ruwan inabi da su. Kuka yabi allolin zinariya
da na azurfa, da na tagulla, da na baƙin ƙarfe, da na itace, da na dutse waɗanda ba
sa ji, ba sa gani, ba sa da gane kome. Amma ba ka girmama Allah ba, wanda ranka
da dukan harkokinka suna a hannunsa. 24 Saboda haka ya aiko da hannun da ya yi
rubutun nan.
25 "Wannan shi ne rubutun da aka yi,

Mene, mene, tekel, farsin

26 "Abin da kalmomin nan suke nufi shi ne,
*"Mene**, Allah ya ƙayyade yawan kwanakin mulkinka ya kuma kawo su ga ƙarshe.
27 *"Tekel*†, An kuma auna ka a ma'auni aka tarar ka kāsa.
28 *"Feres*‡, An raba mulkinka aka ba wa Medes da Farisa."
29 Sai Belshazar ya umarta, aka sa wa Daniyel riga mai shunayya, aka sa sarƙar
zinariya a wuyansa, aka kuma yi shela, cewa yanzu shi ne na uku a cikin masu
mulkin ƙasar.
30 A wannan dare aka kashe Belshazar, sarkin Babiloniyawa,§ 31 Dariyus mutumin
Medes kuwa ya karɓi mulkin, yana da shekara sittin da biyu.

# 6

*Daniyel a cikin ramin zakoki*

1 Ya gamshi Dariyus ya naɗa muƙaddasai 120 su yi shugabanci a duk fāɗin
masarautar, 2 ya naɗa mutum uku a bisa waɗannan muƙaddasan, Daniyel yana ɗaya
daga cikin mutum ukun nan. Sai aka sa muƙaddasan nan a ƙarƙashin waɗannan
uku ɗin domin kada sarki ya yi hasarar kome. 3 To, Daniyel dai ya yi ficce a cikin
shugabannin nan uku har da muƙaddasan ma, saboda waɗansu halaye nagari da
yake da su, wanda ya sa sarki ya yi shiri ya ɗora shi a kan dukan mulkinsa. 4 A kan
haka, shugabannin nan uku da muƙaddasan nan suka yi ƙoƙari su sami wani laifi a
kan Daniyel a yadda yake tafiyar da aikin shugabancinsa, amma ba su samu ba. Ba
su same shi da wani laifin cin hanci ba, domin shi amintacce ne kuma babu wani
aibi a kansa ko rashin kula. 5 A ƙarshe waɗannan mutane suka ce; "Ba za mu taɓa
samun wani laifin da za mu kama Daniyel da shi ba, sai dai ko abin ya shafi dokar
Allahnsa."
6 Saboda haka shugabannin nan suka haɗu da muƙaddasan nan suka tafi wurin
sarki a ƙungiyance suka ce, "Ya Sarki Dariyus, ranka yă daɗe! 7 Shugabannin
masarauta, da masu mulki, da muƙaddasai, da mashawarta da gwamnoni duk sun
amince cewa sarki yă kafa doka yă kuma yi umarni cewa a cikin kwana talatin nan
gaba duk wanda ya yi addu'a ga wani allah ko mutum, in ba a gare ka ba, ya sarki,
jefa shi cikin kogon zakoki. 8 Yanzu, ya sarki, sai ka yi umarni ka kuma yi shi a rubuce

§ **5:22** Ko zuriya; ko magāji * **5:26** Mene yana iya nufin ƙididdigewa Ko kuwa mina (ko kashi na kuɗi).
† **5:27** Tekel yana iya nufin awo Ko kuwa shekel. ‡ **5:28** Feres (jumli ne na Farsin) yana iya nufin an raba Ko
kuwa Farisa Ko kuwa rabin mina Ko kuwa rabin shekel. § **5:30** Ko kuwa Kaldiyawa

saboda kada a canja shi, bisa ga dokar Medes da Farisa, waɗanda ba a iya sokewa.”
9 Sai Sarki Dariyus ya ba da umarnin a rubuce.

10 To, da Daniyel ya ji labarin cewa an fitar da doka, sai ya tafi gidansa a ɗakinsa
na sama inda tagogin ɗakin suke duban wajen Urushalima. Sau uku yakan durƙusa
yă yi addu’a yana yin godiya ga Allahnsa, kamar yadda ya saba yi. 11 Sai waɗannan
mutane suka tafi a ƙungiyance suka kuma iske Daniyel yana addu’a yana roƙon
Allah yă taimake shi. 12 Sai suka tafi wurin sarki suka yi masa magana game da
dokar mulkinsa, suka ce, “Ashe, ba ka yi doka cewa a cikin kwana talatin nan gaba
duk wanda aka tarar yana addu’a ga wani allah ko mutum in ba kai ba, ya sarki, za
ka jefa shi a cikin ramin zakoki ba?”

Sarki ya amsa ya ce, “Dokar tana nan daram bisa ga dokar Medes da Farisa,
waɗanda ba a iya sokewa.”

13 Sai suka ce wa sarki, “Daniyel ɗin nan, wanda yake ɗaya daga cikin waɗanda
aka kwaso daga Yahuda, bai kula da kai ba, ya sarki, balle fa dokar da ka yi. Har
yanzu yana addu’a sau uku a rana.” 14 Da sarki ya ji haka, sai ya damu sosai, ya
ƙudura yă ceci Daniyel, ya yi ta fama har fāɗuwar rana yadda zai yi yă kuɓutar da
shi.

15 Sai mutanen nan suka je wurin sarki a ƙungiyance suka ce masa, “Ka tuna, ya
sarki; cewa bisa ga dokar Medes da Farisa, babu umarni ko dokar da sarki ya yi da
za a iya sokewa.”

16 Saboda haka sai sarki ya ba da umarni suka kuma kawo Daniyel suka jefa shi
cikin ramin zakoki. Sarki ya ce wa Daniyel, “Bari Allahn nan wanda kake bauta masa
kullum, yă cece ka!”

17 Aka kawo dutsen aka rufe bakin ramin, sa’an nan sarki ya hatimce shi da zobensa
da kuma zoban manyan mutanensa, don kada wani yă canja yanayin Daniyel.
18 Sa’an nan sarki ya koma fadarsa ya kwana bai ci ba, kuma babu wata liyafar
da aka kawo masa. Ya kuma kāsa barci.

19 Gari yana wayewa, sai sarki ya tashi ya hanzarta zuwa ramin zakoki. 20 Da ya
yi kusa da ramin zakokin, sai ya kira Daniyel da muryar mai cike da damuwa ya ce,
“Daniyel bawan Allah mai rai, ko Allahn nan naka wanda kake bauta wa kullum, ya
iya cetonka daga zakoki?”

21 Sai Daniyel ya amsa ya ce, “Ran sarki, yă daɗe! 22 Allahna ya aiko da mala’ikansa,
ya kuwa rufe bakunan zakoki. Ba su yi mini rauni ba, gama an same ni marar laifi
ne a gabansa. Ban kuwa taɓa yin wani abu marar kyau a gabanka ba, ya sarki.”

23 Sai sarki ya cika da murna ƙwarai, ya kuma yi umarni a ciro Daniyel daga ramin
zakoki. Kuma da aka fito da Daniyel daga ramin, ba a sami wani rauni a jikinsa ba,
domin ya dogara ga Allahnsa.

24 Sai sarki ya umarta, a kawo mutanen nan da suka yi wa Daniyel maƙarƙashiya,
a tura su, da ’ya’yansu, da matansu cikin ramin zakoki. Kafin ma su kai ƙurewar
ramin, sai zakoki suka hallaka su suka yayyage su, suka yi kaca-kaca da su.

25 Sa’an nan Sarki Dariyus ya rubuta wa dukan mutane, da al’ummai da kuma
mutanen dukan harsunan a duk fāɗin ƙasar.

“Bari yă yi nasara sosai!

26 “Na fitar da doka cewa a cikin dukan iyakar ƙasar mulkina, dole mutane su ji
tsoro su kuma girmama Allah na Daniyel.

“Gama shi ne Allah mai rai
kuma madawwami ne har abada;
ba za a taɓa lalace masarautarsa ba,
mulkinsa kuma ba za tă taɓa ƙarewa ba
27 Yakan kuɓutar ya kuma ceci;
yana yin alamu da al’ajabai

a sama da kuma a duniya.
Shi ya ceci Daniyel
daga ikon zakoki."

28 Daniyel kuwa ya bunkasa a lokacin mulkin Dariyus da kuma mulkin Sairus* na
Farisa.

# 7

*Mafarkin Daniyel na dabbobi huɗu*

1 A shekara ta fari ta mulkin Belshazar sarkin Babilon, Daniyel ya yi mafarki,
wahayoyi kuma suka ratsa tunaninsa a sa'ad da yake a kwance a gadonsa. Sai ya
rubuta abin da mafarkin ya ƙunsa.
2 Daniyel ya ce, "A cikin wahayina da dare na duba, a gabana kuwa ga kusurwoyi
huɗu na sama suna gurɓata babban teku. 3 Sai ga dabbobi huɗu, kowannensu ya yi
dabam da sauran, suna fitowa daga teku.
4 "Na farkon ya yi kamar zaki kuma yana da fikafikai kamar gaggafa. Ina kallo,
sai aka fizge fikafikanta, aka ɗaga ta sama, aka sa ta tsaya a kan ƙafafu biyu kamar
mutum, aka ba ta tunani irin na mutum.
5 "A gabana kuma ga dabba ta biyu, wadda ta yi kamar beyar. Aka ɗaga ta a gefenta
guda, tana kuwa da haƙarƙarai uku a bakinta a tsakanin haƙoranta. Aka faɗa mata,
'Tashi ki cika cikinki da ɗanyen nama!'
6 "Bayan haka, na duba, a gabana kuwa ga wata dabba wadda ta yi kamar Damisa,
a bayanta kuma tana da fikafikai huɗu irin na tsuntsu. Wannan dabbar tana da
kawuna huɗu, aka kuma ba ta iko tă yi mulki.
7 "Bayan haka, a cikin wahayina da dare na duba, a gabana kuwa ga dabba ta
huɗu, wadda take da bantsoro da banrazana da kuma iko ƙwarai. Tana da manyan
haƙoran ƙarfe; ta ragargaje ta cinye abin da ta kama, ta kuma tattaka duk abin da ya
rage a ƙarƙashin ƙafafunta. Ta bambanta da dukan sauran dabbobin da suka riga
ta, tana kuma da ƙahoni goma.
8 "Yayinda nake cikin tunani game da ƙahonin nan, a gabana kuwa ga wani ƙaho,
ɗan ƙanƙani, wanda ya fito daga cikinsu; kuma an tumɓuke uku daga cikin ƙahonin
farko kafin wannan. Wannan ƙaho yana da idanu kamar na mutum da kuma bakin
da yake maganganun fariya.
9 "Ina cikin dubawa,
"sai aka ajiye kursiyoyi,
sai ga wani wanda yake tun fil azal ya zauna a mazauninsa.
Rigarsa ta yi fari fat kamar ƙanƙara;
gashin kansa sun yi fari kamar ulu.
Kursiyinsa kuma harshen wuta,
dukan ƙafafun kursiyin masu kama da keken yaƙin, wuta ne.
10 Kogin wuta yana gudu,
yana fitowa daga gabansa.
Dubun dubbai sun yi masa hidima;
dubu goma sau dubu goma sun tsaya a gabansa.
Aka zauna don shari'a,
aka kuma buɗe littattafai.
11 "Sa'an nan na ci gaba da kallo saboda kalmomin fariyar da wannan ƙaho yake
furtawa. Na yi ta kallo har sai da aka yanke dabbar, aka kuma hallaka jikinta a cikin
wuta. 12 (An tuɓe sauran dabbobin daga mulkinsu, amma aka bar su su rayu na wani
lokaci.)

* **6:28** Ko kuwa Dariyus, wato, mulkin Sairus

13 “A wahayina na dare, na ga a gabana wani kamar ɗan mutum* yana saukowa
tare da gizagizan sama. Ya kusaci Wannan wanda yake Tun fil azal aka kuma kai
shi gabansa. 14 Aka ba shi mulki, daraja da kuma mafificin iko; dukan mutane, da
al’ummai, da mutane daga kowane harshe suka yi masa sujada. Mulkinsa kuwa
dawwammamen mulki ne da ba zai ƙare ba, sarautarsa kuma ba ta taɓa lalacewa.

*Fassarar mafarkin*

15 “Ni, Daniyel, ruhuna ya damu ƙwarai, kuma wahayin da ya ratsa tunanina ya
dame ni. 16 Sai na matsa kusa da ɗaya daga cikin waɗanda suke tsaye a can, na
tambaye shi gaskiya ma’anar waɗannan al’amura.

“Don haka sai ya faɗa mini, ya kuma ba ni fassarar waɗannan al’amura.
17 ‘Waɗannan manyan dabbobi huɗu, Masarautai ne huɗu waɗanda za su taso a
duniya. 18 Amma tsarkaka na Mafi Ɗaukaka za su karɓi wannan sarauta, za su kuwa
mallake ta har abada, I, har abada abadin.’
19 “Sa’an nan kuma sai na so in san ma’anar wannan dabba ta huɗu, wadda ta
yi dabam da sauran dabbobin da suke da matuƙar bantsoro, da take da haƙoran
ƙarfe da kuma farcen tagulla, dabbar ta ragargaje ta cinye abin da ta kama, ta kuma
tattaka duk abin da ya rage a ƙarƙashin ƙafafunta. 20 Na kuma so in gane game da
ƙahonin nan guda goma da suke a kanta da kuma game da ƙahon nan da ya fito,
wanda aka tumɓuke ƙahoni uku a gabansa, ƙahon nan da yake da idanu da bakin da
yake furta manyan maganganun fariya, wanda ya yi kamar ya fi sauran girma. 21 Ina
cikin dubawa, sai ga wannan ƙaho yana yaƙi da tsarkaka yana kuma cin nasara a
kansu, 22 sai da Wannan wanda yake tun fil azal ya zo ya furta hukunci, aka kuma
ba tsarkaka na Mafi Ɗaukaka gaskiya, lokaci kuwa ya cika sai suka karɓi mulki.
23 “Sai ya ba ni wannan bayani, ‘Dabbar nan ta huɗu, ita ce mulki na huɗu da zai
bayyana a duniya. Zai bambanta da dukan sauran mulkoki, zai kuma cinye dukan
duniya, yă tattake ta, yă kuma ragargaje ta. 24 Kahonin nan goma, sarakuna ne goma
waɗanda za su taso daga wannan mulki. Bayansu kuma, wani sarki zai taso, wanda
ya sha dabam da waɗanda suka riga shi. Zai rinjayi sarakunan nan uku. 25 Zai
yi maganar saɓo a kan Mafi Ɗaukaka, zai kuma tsananta wa tsarkaka yă kuma yi
ƙoƙarin sāke lokuta da shari’u. Za a miƙa tsarkaka a hannunsa na wani lokaci, lokuta
da kuma rabin lokaci.†
26 “ ‘Amma majalisa za tă yi zama, za a karɓe ikonsa, a kuma hallaka shi gaba
ɗaya har abada. 27 Sa’an nan za a ba da mulki, iko da girma na mulkokin da suke
a ƙarƙashin dukan sammai ga tsarkaka, mutane na Mafi Ɗaukaka. Mulkinsa kuwa
mulki ne marar matuƙa, kuma dukan masu mulki za su yabe shi, su kuma yi masa
biyayya.’
28 “Wannan shi ne ƙarshen batun. Ni, Daniyel na damu ƙwarai da irin tunanina,
kuma fuskata ta rikice, amma na riƙe batun a zuciyata.”

# 8

*Wahayin Daniyel a kan rago da akuya*

1 A shekara ta uku ta mulkin sarki Belshazar, ni, Daniyel, na ga wahayi, bayan
wancan da na riga gani. 2 A cikin wahayin, na ga kaina a mafakar Shusha a yankin
Elam; a wahayin na ga ina a bakin Kogin Ulai. 3 Na ɗaga ido, a gabana kuwa sai ga
rago mai ƙahoni biyu, yana tsaye a gefen mashigin kogin, ƙahonin kuma suna da
tsawo. Ɗaya daga cikin ƙahonin ya fi ɗayan tsawo. Wanda ya fi tsawon shi ne ya

* **7:13** Kalmomin Arameyik nan *bar enash* suna nufin mutum. Kalmomin nan ɗan mutum an yi amfani da su a nan saboda a amfanin da aka yi da su a Sabon Alkawari a matsayi wakilin suna na Yesu, mai yiwuwa saboda dangane a kan wannan ayar. † **7:25** Ko kuwa na shekara biyu da rabi

tsiro daga baya. 4 Na lura da ragon sa'ad da ya kai karo wajen yamma da arewa da
kudu. Babu wata dabbar da ta iya ƙarawa da shi, babu kuma wanda ya iya kuɓuta
daga ikonsa. Ya yi yadda ya ga dama, ya kuma zama mai girma.

5 Yayinda nake tunani game da wannan, farat ɗaya sai ga bunsurun da yake da
sanannen ƙaho tsakanin idanunsa ya ɓullo daga wajen yamma, yana ratsa dukan
duniya ba ya ko taɓa ƙasa. 6 Ya zo wajen rago mai ƙahoni biyu ɗin nan da na riga na
gani tsaye a gefen mashigin kogin nan ya tasar masa da fushi mai zafi. 7 Na ga ya zo
kusa da ragon, ya husata da shi ƙwarai, ya kai wa ragon hari. Ya kakkarya ƙahoninsa
nan biyu. Karfin ragon ya kāsa, bai iya kāre kansa daga bunsurun ba. Bunsurun ya
buge shi ƙasa ya tattake shi. Ba wanda ya iya ceton ragon daga bunsurun. 8 Bunsurun
kuwa ya ƙasaita, amma a ƙwanƙolin ikonsa sai aka karye babban ƙahonsa, kuma
a wurin da ƙahon nan ya kasance waɗansu sanannun ƙahoni huɗu suka tsiro suna
fuskantar kusurwoyin nan huɗu.

9 Daga cikin ɗayansu kuma wani ƙaramin ƙaho ya fito, ya yi girma ya ƙasaita
ƙwarai zuwa kudu da kuma gabas da wajen Kyakkyawar Kasa. 10 Ya yi girma
sai da ya kai rundunar sammai, ya kuma fid da waɗansu rundunar taurari zuwa
ƙasa ya kuma tattake su. 11 Sai ya ɗora kansa ya zama mai girma kamar Sarkin
runduna; sai aka ɗauke hadaya ta kullayaumi daga gare shi, aka kuma saukar da
wurin masujadarsa ƙasa. 12 Saboda tawaye, sai aka ba da rundunar tsarkaka* da
kuma hadayar ƙonawa ta kowace rana ga ƙahon. Sai ya yi watsi da gaskiya, ya yi
abin da ya ga dama, ya kuwa yi nasara.

13 Sa'an nan na ji mai tsarkin nan yana magana, wani mai tsarki kuma ya ce
da wancan, "Har yaushe wannan wahayi zai tabbata, wahayi game da hadaya ta
kullayaumi, da tawayen da yake kawo lalacewa, da kuma miƙa wuri mai tsarki da
kuma na rundunar da za a tattake a ƙarƙashin sawu?"
14 Sai ya ce mini, "Zai ɗauki safiya da yamma 2,300; sa'an nan za a sāke tsarkake
wuri mai tsarki."

### *Fassarar wahayin*

15 Yayinda ni, Daniyel, nake duban wahayi ina ƙoƙari in fahimce shi, sai ga wani
a gabana wanda ya yi kama da mutum. 16 Sai na ji muryar wani mutum daga Ulai
tana cewa, "Jibra'ilu, faɗa wa wannan mutum ma'anar wahayin."

17 Da ya zo kusa da inda nake tsaye, na firgita na kuma fāɗi rubda ciki. Ya ce da
ni "Dan mutum, ka gane da cewa wannan wahayi yana magana ne a kan kwanakin
ƙarshe."
18 Yayinda yake magana da ni, barci mai nauyi ya kwashe ni, da nake kwance rubda
ciki. Sai ya taɓa ni ya kuma tashe ni tsaye.

19 Sai ya ce, "Zan faɗa maka abin da zai faru a lokacin fushi, saboda wahayin yana
magana ne a kan lokacin da aka ƙayyade na ƙarshe.† 20 Rago mai ƙahoni biyu da ka
gani, yana a madadin sarakunan Medes da Farisa ne. 21 Bunsurun kuwa sarkin Girka
ne, kuma babban ƙahon da yake tsakanin idanunsa, sarki na farko ne. 22 Kahoni
huɗu da suka maya wannan da ya karye yana a madadin masarautu huɗu da za su
tashi daga cikin al'ummarsa amma ba za su sami irin ikonsa ba.

23 "Can wajen ƙarshe mulkinsu, sa'ad da muguntarsu ta kai intaha, wani mugun
sarki mai rashin hankali, uban makirci, zai fito. 24 Zai yi ƙarfi ƙwarai da gaske, amma
ba da ikonsa ba. Zai jawo mummunar hallakarwa kuma zai yi nasara a duk abin da
ya sa gaba. Zai hallakar da majiya ƙarfi da kuma tsarkaka. 25 Zai sa yaudara ta ƙara
yin yawa, zai ɗaukaka kansa. Sa'ad da suke ji sun sami mafaka, zai hallaka mutane

---

* **8:12** ko tawayen, mayaƙan † **8:19** Ko kuwa domin ƙarshen zai zama a ƙayyadadden lokaci

da yawa sa'an nan kuma yă fara gāba da Sarkin sarakuna. Duk da haka za a hallaka
shi, amma ba da ikon mutum ba.
26 "Wahayin nan na safiya da yamma da aka nuna maka gaskiya ne, amma ka ɓoye
wahayin, gama ya shafi nan gaba mai tsawo ne."
27 Ni, Daniyel, na gaji matuƙa na kuma yi rashin lafiya na kwanaki masu yawa.
Sa'an nan sai na tashi na ci gaba da hidimar sarki. Wahayin ya shige mini duhu, ya
fi ƙarfin fahimtata.

# 9

*Addu'ar Daniyel*

1 A shekara ta fari da mulkin Dariyus ɗan Zerzes* (wanda yake Bamediye), wanda
aka mai da shi sarki a masarautar Babiloniyawa† 2 a shekara ta farko ta mulkinsa,
ni, Daniyel na gane daga cikin littattafai, bisa ga maganar UBANGIJI da aka faɗa wa
annabi Irmiya, cewa zaman Urushalima kango zai kai shekara saba'in. 3 Sai na juya
wurin Ubangiji Allah na roƙe shi ta wurin addu'a da koke-koke, cikin azumi, ina saye
da tsummoki, na kuma zauna a cikin toka.
4 Na yi addu'a ga UBANGIJI Allahna na furta laifina.

"Ya Ubangiji, mai alfarma da kuma Allah mai banrazana, wanda yake cika
alkawarinsa na ƙauna ga duk wanda ya ƙaunace shi ya kuma kiyaye dokokinsa,
5 mun yi zunubi muka kuma yi ba daidai ba. Mu mugaye ne da kuma 'yan tawaye;
mun juya wa umarninka da shari'unka baya. 6 Ba mu saurari bayinka annabawa
ba, waɗanda suka yi magana a sunanka ga sarakunanmu da masu mulkinmu da
iyayenmu, da kuma dukan mutanen ƙasa.
7 "Ubangiji, kai mai adalci ne, amma a yau kunya ta rufe mu, mutanen Yahuda
da mutanen Urushalima da na dukan Isra'ila, waɗanda suke kusa da kuma nesa,
a dukan ƙasashen da ka warwatsa mu saboda rashin amincinmu a gare ka. 8 Ya
UBANGIJI, mu da sarakunanmu, da masu mulkinmu da iyayenmu kunya ta rufe mu
saboda mun yi maka zunubi. 9 Ubangiji Allahnmu mai jinƙai ne, mai gafartawa ne
kuma, ko da yake mun yi masa tawaye; 10 ba mu yi biyayya ga UBANGIJI Allahnmu
ba, ba mu kuma kiyaye shari'unsa da ya ba mu ta wuri bayinsa annabawa ba.
11 Dukan Isra'ila sun karya dokokinka suka kuma juya maka baya, sun ƙi yi maka
biyayya.

"Saboda haka la'anoni da rantsuwar hukunce-hukuncen da suke a rubuce a cikin
Dokar Musa, bawan Allah, sun kama mu domin mun yi maka zunubi. 12 Ka cika
kalmomin da ka yi a kanmu da kuma a kan masu mulkinmu ta wurin kawo mana
babban bala'i. A duniya duka ba a taɓa yin wani abu kamar yadda aka yi wa
Urushalima ba. 13 Kamar yadda yake a rubuce cikin Dokar Musa, dukan wannan
bala'i ya sauko a kanmu, duk da haka ba mu nemi tagomashin UBANGIJI Allahnmu
ta wurin barin aikatawa zunubanmu, mu kuma mai da hankali a kan gaskiyarka ba.
14 UBANGIJI bai yi wata-wata wajen kawo mana bala'i ba, domin UBANGIJI Allahnmu
mai adalci ne a cikin dukan abin da yake yi; duk da haka ba mu yi masa biyayya
ba.
15 "Yanzu, ya Ubangiji Allahnmu, wanda ya fito da mutanensa daga Masar ta
hannu mai ƙarfi wanda kuma ya yi wa kansa sunan da ya dawwama har yă zuwa
yau, mun yi zunubi, mun yi abin da ba daidai ba. 16 Ya Ubangiji, ta wurin kiyaye
dukan ayyukanka na adalci, ka huce daga fushinka da hukuncinka da ka yi a kan
Urushalima, birninka, tudunka mai tsarki. Zunubinmu da laifofin iyayenmu sun
mai da Urushalima da kuma mutanenka abin ba'a ga dukan waɗanda suke kewaye
da mu.

* **9:1** Da Ibraniyanci Ahasuwerus † **9:1** Ko kuwa Kaldiyawa

17 “Yanzu, ya Allahnmu, ka ji addu’o’i da koke-koken bayinka. Saboda sunanka,
ya Ubangiji, ka duba da rahama wurinka mai tsarki da ya zama kango. 18 Ka kasa
kunne, ya Allah, ka kuma ji; ka buɗe idanunka ka kuma ga yadda birninka ya
zama kango, birnin da yake ɗauke da Sunanka. Ba cewa muna roƙonka saboda
mu masu adalci ba ne, amma saboda girman jinƙanka. 19 Ya Ubangiji, ka saurara!
Ya Ubangiji ka gafarta! Ya Ubangiji, ka ji ka kuma yi wani abu! Saboda sunanka, ya
Allahna, kada ka yi jinkiri, domin da sunanka ake kiran birninka da jama’arka.”

*Annabci a kan Mako Saba’in*

20 Yayinda da nake magana da addu’a, ina furta zunubina da zunubin mutanena
Isra’ila ina miƙa koke-kokena ga Ubangiji Allahna saboda tudunsa mai tsarki,
21 yayinda nake cikin addu’a, sai Jibra’ilu, mutumin nan da na gani a wahayin da
ya wuce, ya zo wurina gaggauce wajen lokacin yin hadaya ta yamma. 22 Ya umarce
ni ya kuma ce mini, “Daniyel, yanzu na zo domin in ba ka hikima da ganewa. 23 Da
zarar ka fara addu’a, an amsa, wadda na zo in faɗa maka, gama ana ƙaunar ka sosai.
Saboda haka, ka yi lura da saƙon ka kuma fahimci wahayin.

24 “An ƙayyade wa jama’arka da tsattsarkan birninka shekara ɗari huɗu da tasa’in
domin a kawo ƙarshen laifi da zunubi, domin a yi kafarar laifi, sa’an nan a shigo da
adalci madawwami, a rufe wahayi da annabci, a tsarkake haikali.

25 “Sai ka sani ka kuma fahimci wannan; Tun daga sa’ad da aka kafa doka‡ don a
maido a kuma sāke gina Urushalima har sai Shafaffen nan,§ mai mulki, ya zo, za a
yi shekara arba’in da tara, da shekara ɗari huɗu da talatin da huɗu. Za a sāke gina
ta a yi mata tituna da mafaka. 26 Bayan shekara ɗari huɗu da talatin da huɗu, za a
datse Shafaffen nan zai kuma kasance ba shi da kome.* Mutanen mai mulkin za su
zo su hallaka birnin da kuma wuri mai tsarki. Karshen zai zo kamar rigyawa. Yaƙi
zai ci gaba har ƙarshe, a kuma hallakar kamar yadda aka ƙaddara. 27 Zai tabbatar
da alkawari da mutane masu yawa har na shekara bakwai.† A tsakiyar bakwai ɗin
nan ɗaya‡ zai kawo ƙarshen duk wata hadaya da baiko. Kuma a kusurwar haikali
zai sa abin ƙyama mai kawo hallaka, har sai ƙarshen da aka ƙaddara ya auko wa
wanda ya sa abin ƙyama.”§,*

# 10

*Wahayin Daniyel na mutum*

1 A shekara ta uku ta Sairus sarkin Farisa, sai aka ba wa Daniyel (wanda ake kira
Belteshazar) wahayi. Saƙon kuwa gaskiya ce wadda take tattare da babban yaƙi.
Fahimtar saƙon ya zo masa a cikin wahayi.

2 A wannan lokaci ni Daniyel na yi makoki har na sati uku. 3 Ban ci abinci mai
kyau ba; ba nama ko ruwa inabin da ya shiga bakina; kuma ba na amfani da man
shafawa gaba ɗaya har sai da sati nan uku suka wuce.

4 A rana ta ashirin da huɗu ga watan farko, a sa’ad da nake tsaye a bakin babban
kogi, Tigris, 5 na ɗaga kaina na duba sai ga wani mutum tsaye sanye da rigar lilin, ya
yi ɗamara da zinariya zalla daga Ufaz kewaye da ƙugunsa. 6 Jikinsa kamar lu’ulu’u
yake, fuskarsa kuma kamar walƙiya, idanunsa kamar harshen wuta, hannuwansa
da ƙafafunsa kamar gogaggiyar tagulla, muryarsa kuma kamar amon babban taron
jama’a.

‡ **9:25** Ko kuwa kalma § **9:25** Ko kuwa shafaffen nan; haka kuma a aya 26 * **9:26** Ko kuwa ba zai kasance da kome ba; Ko kuwa a kawar, amma ba don kansa ba † **9:27** Ko kuwa “mako” ‡ **9:27** Ko kuwa “mako” § **9:27** Ko kuwa shi (abin da ba mutum ba) * **9:27** Ko kuwa abin da zai kawo hallaka zai zo ne a kan ƙwanƙolin za tă zubo allahn birnin

7 Ni, Daniyel, kaɗai ne na ga wahayin; mutanen da suke tare da ni ba su gani ba,
amma wata irin babbar razana ta auko musu har suka gudu suka ɓuya. 8 Sai aka
bar ni ni kaɗai, ina juyayi wannan babban wahayi, ba ni da sauran ƙarfi, fuskata ta
yamutse kuma ba ni da sauran ƙarfi. 9 Sai na ji yana magana, da ina sauraronsa, sai
na shiga barci mai nauyi, na kuwa fāɗi rubda ciki.
10 Sai hannu ya taɓa ni ya sa makyarkyata a hannuna da ƙafafuna. 11 Sai ya ce,
"Daniyel, kai ne wanda ake ƙauna sosai, ka yi lura da kyau game da kalmomin da
zan yi maka magana a kansu, ka tashi yanzu, gama an aiko ni a gare ka." Sa'ad da
ya faɗa mini haka, sai na tashi a tsaye ina rawan jiki.
12 Sai ya ci gaba da cewa, "Kada ka ji tsoro, Daniyel. Gama tun daga ran da ka fara
sa zuciya ga neman ganewa, ka kuma ƙasƙantar da kanka a gaban Allahnka, an ji
addu'arka, amsar addu'arka ce ta kawo ni. 13 Amma mai mulkin masarautar Farisa
ya tsare ni har kwana ashirin da ɗaya. Sai da Mika'ilu, ɗaya daga cikin manya
shugabanni, ya zo ya taimake ni, saboda an tsare ni a can tare da sarkin Farisa.
14 Yanzu na zo domin in bayyana maka abin da zai faru da mutanenka nan gaba,
gama wahayin ya shafi lokacin da bai riga ya zo ba ne."
15 Yayinda yake faɗin mini haka, sai na sunkuyar da kaina ƙasa shiru, ba magana.
16 Sai wani wanda ya yi kama da mutum* ya taɓa leɓunana, na kuma buɗe bakina sai
na fara magana. Na ce wa wannan da yake tsaye a gabana, "Na cika da azaba saboda
wannan wahayi, ranka yă daɗe, ina kuma neman taimako. 17 Yaya ni bawanka zan
iya magana da kai, ranka yă daɗe? Karfina ya ƙare kuma ina numfashi da ƙyar."
18 Har yanzu wannan wanda yana kama da mutum ya taɓa ni ya kuma ba ni ƙarfi.
19 Ya kuma ce, "Kada ka ji tsoro, ya kai mutumin da ake fahariya, salama a gare ka!
Ka ƙarfafa yanzu; ka yi ƙarfin hali."
Sa'ad da ya yi magana da ni, sai na samu ƙarfi na ce, "Ka yi magana ranka yă daɗe,
tun da yake ka sa na sami ƙarfi."
20 Sai ya ce mini, "Ka san abin da ya kawo ni gare ka? Ba da jimawa ba zan koma
in yi yaƙi da mai mulkin Farisa, kuma idan na tafi, mai mulkin Hellenawa zai taso;
21 amma da farko zan faɗa maka abin da aka rubuta a cikin Littafin Gaskiya (Babu
wanda ya taimake ni yaƙi da waɗannan sai dai Mika'ilu, sarkinku.

# 11

1 A shekara ta fari ta Dariyus mutumin Mede, na ɗauki matsayina domin in goyi
baya in kuma kāre shi.)

### *Sarakunan kudu da arewa*

2 "Yanzu dai, zan faɗa maka gaskiya. Sarakuna uku za su taso a Farisa, sa'an nan
kuma na huɗu, wanda zai fi dukansu dukiya. Sa'ad da zai sami iko saboda dukiyarsa,
zai zuga dukan kowane mutum yă yi gāba da masarautar Girka. 3 Sa'an nan wani
babban sarki zai bayyana, wanda zai yi mulki da babban iko yă kuma yi abin da
ya ga dama. 4 Bayan da ya bayyana, daularsa za tă wargaje za a rarraba ta zuwa
kusurwoyi huɗu na duniya, a ba waɗansu waɗanda ba zuriyarsa ba, ba kuwa za su
yi mulki da iko kamar yadda ya yi ba, gama za a tumɓuki daularsa a kuma ba wa
waɗansu.
5 "Sai sarki Kudu zai yi ƙarfi ƙwarai, amma ɗaya daga cikin komandodinsa zai yi
ƙarfi fiye da shi, zai kuma yi mulki masarautarsa da iko mai girma. 6 Bayan 'yan
shekaru, za su haɗa kai. Diyar sarkin Kudu za tă je wurin sarkin Arewa ta sada
zumunci, amma ba za tă riƙe iko ba, shi kuwa da ikonsa* ba za su daɗe ba. A

* **10:16** Yawancin rubuce-rubucen hannu na Nassin Masoretik; ɗaya daga cikin rubuce-rubucen Masoretik, Naɗaɗɗen littafin Mataccen Teku da kuma Seftuwajin Sa'an nan wani abu kamar hannun mutum * **11:6** Ko kuwa zuriyarsa

waɗannan kwanaki za a bashe ta, da ita da masu rakiyarta da kuma mahaifinta† da
kuma wanda ya goyi bayanta.

7 “Wani daga cikin zuriyarta zai taso yă ɗauki matsayinta. Zai kai wa sojojin sarkin
Arewa hari yă kuma shiga kagararsa; zai yi yaƙi da su yă kuma yi nasara. 8 Zai ƙwace
allolinsu, siffofinsu na ƙarfe da kuma kaya masu daraja na azurfa da na zinariya a
kuma kai su Masar. Zai yi ’yan shekaru bai kai wa sarkin Arewa yaƙi ba. 9 Sa’an
nan sarkin Arewa zai kai wa sarkin Kudu hari, amma zai janye, yă koma ƙasarsa.
10 ’Ya’yansa maza za su yi shirin yaƙi za su kuma tattara babbar rundunar sojoji,
waɗanda za su yi ta mamayewa kamar rigyawar da ba iya tarewa, kuma za su kai
yaƙin har kagararsa.

11 “Sa’an nan sai sarkin Kudu zai kama hanya da fushi zuwa yaƙi da sarkin Arewa,
wanda zai tattara babbar rundunar yaƙi, amma za a ci shi da yaƙi. 12 Sa’ad da zai
kawar da rundunar, sarkin Kudu zai cika da girman kai zai kuma kashe mutane
dubbai, duk da haka ba zai kasance mai nasara ba. 13 Sarki Arewa kuma zai ƙara
tara babbar rundunar soja, wadda ta fi ta dā girma; bayan waɗansu shekaru kuma,
zai tafi yaƙi da babbar rundunar mayaƙa cike da kayan yaƙi.

14 “A waɗannan lokutan mutane da yawa za su tashi gāba da sarkin Kudu. Amma
waɗansu ’yan kama-karya za su taso daga jama’arka da niyya su cika abin da
wahayin ya ce, amma za a fatattake su. 15 Sa’an nan sarkin arewa zai zo ya gina
mahaurai a jikin katagar birni don yă ci birnin da yaƙi. Sojojin nan na Kudu kuwa
ba za su iya tsayawa ba, ko zaɓaɓɓun jarumawansu ma, gama za su rasa ƙarfin
tsayawa. 16 Wanda ya kai harin zai yi yadda ya ga dama, ba wanda zai iya ja da
shi. Zai kafa kansa a Kyakkyawar Kasa zai kuma sami ikon da zai hallaka ta. 17 Zai
yunƙura yă zo da ƙarfin dukan masarautarsa zai kuma nemi haɗinkan sarkin Kudu.
Zai kuma ba shi diyarsa yă aura don yă lalatar da mulkin, amma shirinsa‡ ba zai yi
nasara ba ko yă taimake shi ba. 18 Sa’an nan zai mai da hankalinsa zuwa ƙasashe
a bakin kogi, zai kuma kama da yawansu, amma wani komanda zai kawo ƙarshen
faɗin ransa, zai kuma sa faɗin ransa yă koma masa. 19 Bayan wannan, zai juya ga
kagarar ƙasarsa, amma zai yi tuntuɓe yă fāɗi, ba kuwa za a ƙara ganinsa ba.

20 “Magājinsa zai aiki mai karɓar haraji don darajar masarautarsa. Amma ba da
daɗewa ba za a hallaka shi, duk da haka ba da fushi ko cikin yaƙi ba.

21 “Magājin wannan sarki zai zama wani mutumin banza wanda ma bai fito daga
gidan sarauta ba. Zai taso ba zato ba tsammani, yă ƙwace sarautar ta hanyar zamba.
22 Sa’an nan zai shafe mayaƙa masu yawa a gabansa; zai hallaka har da waɗanda suke
mulki na alkawari. 23 Bayan ƙulla yarjejjeniya da shi, zai yi zamba cikin aminci, kuma
zai sami damar hawan mulki da goyon baya mutane kaɗan. 24 Sa’ad da yankuna mafi
arziki suke ji kome lafiya yake, zai kai musu hari kuma Zai aikata abin da kakanninsa
ba su taɓa yi ba. Zai rarraba abin da aka kwaso daga yaƙi, da ganima, da dukiya ga
dukan mabiyansa. Zai kuma yi shiri yă kai wa mafaka hari, amma na ɗan lokaci ne
kawai.
25 “Tare da babbar rundunar mayaƙa zai yi ƙarfin hali yă far wa sarkin Kudu da
yaƙi. Sarkin kudu zai haɗa babbar rundunar soja mai ƙarfi don yaƙin, amma ba zai
iya karo da shi ba, domin za a shirya masa maƙarƙashiya. 26 Waɗanda suke ci daga
tanadin sarki za su yi ƙoƙari su hallaka shi; za a share mayaƙansa, kuma za a kashe
mutane masu yawa a yaƙin. 27 Sarakunan nan biyu sun sa mugunta a ransu. Za su
zauna a tebur guda su yi ta shara wa juna ƙarya, amma a banza, gama lokacin da
aka ƙayyade bai yi ba tukuna.

† **11:6** Ko kuwa yaro (dubi Bulget da Siriyak) ‡ **11:17** Ko kuwa amma ita

28 “Sarkin Arewa zai koma ƙasarsa da dukiya mai girma, amma zuciyarsa za tă
yi gāba da tsattsarkan alkawari. Zai ɗauki mataki a kan wannan abu sa’an nan yă
koma ƙasarsa.
29 “A ƙayyadadden lokaci zai sāke kai wa Kudu hari, amma a wannan karo abin da
zai faru zai sha bamban daga abin da ya faru can baya. 30 Jiragen ruwa yammancin
bakin teku§ za su yi gāba da shi, zuciyarsa kuwa za tă yi sanyi. Sa’an nan zai juya
ya huce haushinsa a kan tsattsarkan alkawari. Zai komo yă nuna jinƙai ga waɗanda
suka juya wa tsattsarkan alkawari baya.
31 “Mayaƙansa za su taso su ƙazantar da kagarar haikali za su kuma kawar da
hadaya ta kullum. Sa’an nan za su kafa abin banƙyama da yake lalatarwa. 32 Ta
wurin daɗin baki zai gurɓata waɗannan da suka karya alkawari, amma mutanen da
suka san Allahnsu za su yi tsayin daka su yi jayayya da shi.
33 “Waɗanda suke da hikima za su wayar da kan mutane da yawa, duk da haka za
a kashe su da takobi, waɗansu da wuta, a washe waɗansu a kai su bauta. 34 Sa’ad da
suka fāɗi, za su sami ɗan taimako, mutane da yawa za su haɗa kai da su, amma da
munafunci. 35 Waɗansu masu hikima za su yi tuntuɓe, don a tsabtacce su, a tsarkake
su, su yi tsab, har matuƙar da aka ƙayyade ta yi.

*Sarkin da ya ɗaukaka kansa*

36 “Sarkin zai yi abin da ya ga dama. Zai ɗaukaka yă kuma girmama kansa gaba
da kowane allah zai kuma faɗa munanan abubuwa a kan Allahn alloli. Zai yi nasara
har sai lokacin hukunci ya cika, gama abin da aka ƙaddara zai cika. 37 Ba zai kula da
alloli iyayensa ba ko wanda mata suke sha’awa, balle ma yă ga darajar wani allah,
amma zai ɗaukaka kansa gaba da su duka. 38 A maimakonsu, zai ɗaukaka allahn
kagarai; allahn da kakanninsa ba su ko sani ba, shi ne zai miƙa masa zinariya, da
azurfa, da duwatsu masu daraja, da abubuwa masu tsada. 39 Zai kai wa kagarai mafi
ƙarfi hari da taimakon baƙon allah zai kuma girmama waɗanda suka yarda da shi
zai ba su girma, ya kuma shugabantar da su a kan mutane da yawa, zai raba musu
ƙasa ta zama ladansu.*
40 “A lokaci ƙarshe sarkin Kudu zai tasar masa da yaƙi, sarkin Arewa kuwa zai
tunzura, yă tasar masa da kekunan yaƙi da mahayan dawakai, da jiragen ruwa da
yawa. Zai ratsa ƙasashe, yă ci su da yaƙi, yă wuce. 41 Zai kuma mamaye Kyakkyawa
Kasa. Kasashe masu yawa za su fāɗi, amma Edom, Mowab da kuma shugabannin
Ammon za su kuɓuta daga hannunsa. 42 Zai fadada mulkinsa har zuwa ƙasashe
masu yawa; Masar ma ba za tă tsira ba. 43 Zai mallaki dukiyoyi na zinariya, da na
azurfa, da dukan abubuwa masu tsada na Masar. Zai kuma ci Libiyawa da Kush da
yaƙi. 44 Amma labari daga gabas da arewa za su firgita shi, shi kuwa zai ci gaba da
yin yaƙi da zafi, yă karkashe mutane da yawa, yă shafe su. 45 Zai kafa tentin mulkinsa
tsakanin tekunan da suke† a kyakkyawan tsauni mai tsarki. Duk da haka zai zo ga
ƙarshensa, kuma babu wanda zai taimake shi.

# 12

*Karshe zamani*

1 “A wannan lokaci Mika’ilu, babban mai mulki wanda yake kāre mutanenka, zai
tashi. Za a yi lokacin matsananciyar wahala wanda ba a taɓa yi tun farkon ƙasashe
har zuwa yanzu. Amma a lokacin da mutanenka, kowane mutum wanda aka sami
sunansa a rubuce a cikin littafin, za a cece shi. 2 Dumbun mutanen da suka yi barci
cikin turɓayar duniya za su farka, waɗansu zuwa ga rai madawwami, waɗansu
zuwa ga madawwamiyar kunya da kuma madawwamin ƙasƙanci. 3 Waɗanda suke

§ **11:30** Da Ibraniyanci na Kittim * **11:39** Ko kuwa ƙasar don lada † **11:45** Ko kuwa teku da

da hikima[*] za su haskaka kamar hasken samaniya, waɗanda kuma suka jagoranci
waɗansu da yawa zuwa adalci, za su zama kamar taurari har abada abadin. 4 Amma
kai, Daniyel, ka rufe zancen nan ka kuma liƙe kalmomin littafin nan har sai ƙarshe.
Mutane da yawa za su yi ta kai komo don neman sani."

5 Sa'an nan ni, Daniyel, na duba, a gabana kuwa ga waɗansu mutum biyu tsaye,
ɗaya a wannan hayen kogi ɗaya kuma a ƙetaren kogin. 6 Dayansu ya ce wa mutumin
da yake sanye da tufafin lilin, wanda yake a saman ruwan kogin, "Har yaushe
waɗannan abubuwan banmamakin za su cika?"
7 Mutumin da yake sanye da tufafin lilin, wanda yake a saman ruwan kogin, ya ɗaga
hannun damansa da kuma na hagunsa sama, sai na ji yana rantsuwa da wannan da
yake raye har abada, yana cewa, "Zai kasance na ɗan lokaci, lokuta da rabin lokaci.[†]
Za a kammala waɗannan abubuwa, sa'ad da aka gama ragargaje ikon tsarkakan
mutane."
8 Na kuma ji, amma ban fahimta ba. Don haka sai na yi tambaya, "Ranka yǎ daɗe,
mene ne ƙarshen waɗannan abubuwa?"
9 Sai ya amsa ya ce, "Ka kama hanyarka, Daniyel, domin a rufe kalmomin aka
kuma liƙe su har sai ƙarshen lokaci. 10 Za a tsarkake mutane da yawa, za a maishe
su marasa aibi a kuma tace su; amma mugaye za su ci gaba da mugunta. Babu wani
mugun da zai fahimta, amma waɗanda za su zama masu hikima za su fahimta.
11 "Daga lokacin da za a hana miƙa hadayar ƙonawa ta yau da kullum, a kuma
kafa abin banƙyama, wanda yake lalatarwa, za a yi kwana 1,290. 12 Mai albarka ne
wanda ya jira har yǎ zuwa ƙarshen kwanakin nan 1,335.
13 "Gare ka dai, ka yi tafiyarka har zuwa ƙarshe. Za ka huta, sa'an nan a ƙarshen
kwanaki za ka tashi don karɓi sashen gadon da aka ba ka."

* **12:3** Ko kuwa waɗanda suke ba da hikima † **12:7** Ko kuwa shekara, shekara biyu da kuma rabi shekara

# Hosiya

1 Maganar UBANGIJI da ta zo wa Hosiya ɗan Beyeri a zamanin mulkin Uzziya, Yotam,
Ahaz da Hezekiya, sarakunan Yahuda, da zamanin mulkin Yerobowam ɗan Yowash*
sarkin Isra'ila.

*Matar Hosiya da 'ya'yanta*

2 Sa'ad da UBANGIJI ya fara magana ta wurin Hosiya, UBANGIJI ya ce masa, "Ka tafi,
ka auro wa kanka mazinaciya da 'ya'yan da aka haifa ta hanyar rashin aminci, domin
ƙasar tana da laifin mummunan zina ta wurin rabuwa da UBANGIJI." 3 Saboda haka
sai ya auri Gomer 'yar Dibilayim, ta kuwa yi ciki ta haifi ɗa namiji.
4 Sai UBANGIJI ya ce wa Hosiya, "Ka ba shi suna Yezireyel, domin ba da daɗewa ba
zan hukunta gidan Yehu saboda kisan da aka yi a Yezireyel, zan kuma kawo ƙarshen
mulkin Isra'ila. 5 A wannan rana zan karye ƙarfin Isra'ila a Kwarin Yezireyel."
6 Gomer ta sāke ɗauki ciki ta kuma haifi 'ya mace. Sai UBANGIJI ya ce wa Hosiya,
"Ka ba ta suna, Lo-Ruhama,† gama ba zan ƙara nuna wa gidan Isra'ila ƙauna ba, har
da zan gafarta musu. 7 Duk da haka zan nuna ƙauna ga gidan Yahuda; zan kuma
cece su, ba da baka, takobi ko yaƙi ba, ko ta wurin dawakai, ko masu hawan dawakai
ba, sai ko ta wurin UBANGIJI Allahnsu."
8 Bayan ta yaye Lo-Ruhama, sai Gomer ta sāke haifi wani ɗa namiji. 9 Sai UBANGIJI
ya ce, "Ka ba shi suna Lo-Ammi,‡ gama ku ba mutanena ba ne, ni kuma ba Allahnku
ba ne.
10 "Duk da haka Isra'ilawa za su zama kamar yashi a bakin teku, da ba za a iya
aunawa ko a ƙirga ba. A inda aka ce musu, 'Ku ba mutanena ba ne,' za a kira su
''ya'yan Allah mai rai.' 11 Mutanen Yahuda da mutanen Isra'ila za su sāke haɗu su
zama ɗaya, za su kuma naɗa shugaba guda su kuma fita daga ƙasar, gama ranar za
tă zama mai girma wa Yezireyel.

## 2

1 "Ka ce da 'yan'uwanka maza, 'Mutanena,' ka kuma ce da 'yan'uwanka mata,
'Kaunatacciyata.'

*An hukunta an kuma mayar da Isra'ila*

2 "Ka tsawata wa mahaifiyarka, ka tsawata mata,
gama ita ba matata ba ce,
ni kuma ba mijinta ba ne.
Ku roƙe ta tă daina karuwancinta
da kuma rashin aminci a tsakanin nononta.
3 In ba haka ba zai tuɓe ta tsirara
in bar ta kamar yadda take a ranar da aka haife ta;
zan sa ta zama kamar hamada,
in mayar da ita busasshiyar ƙasar,
in kashe ta da ƙishirwa.
4 Ba zan nuna wa 'ya'yanta ƙaunata ba,
domin su 'ya'yan zina ne.
5 Mahaifiyarsu ta yi rashin aminci
ta kuma ɗauki cikinsu ta wurin yi abin kunya.

* 1:1 Da Ibraniyanci Yowash, wani suna na Yehowash † 1:6 Lo-Ruhama yana nufin ba tausayi. ‡ 1:9 Lo-Ammi yana nufin ba mutanena ba.

Ta ce, ‘Zan bi kwartayena,
waɗanda suke ba ni abinci da ruwa,
ulu nawa da lilina, mai nawa da kuma abin sha na.’
6 Saboda haka zai tare hanyarta da ƙaya;
zan yi mata katanga don kada tă sami hanya.
7 Za tă bi kwartayenta amma ba za tă kama su ba;
za tă neme su amma ba za tă same su ba.
Sa’an nan za tă ce,
‘Zan koma ga mijina na fari,
gama dā ya fi mini yadda nake a yanzu.’
8 Ba ta yarda cewa ni ne
wanda ya ba ta hatsi, sabon ruwan inabi da mai ba,
wanda ya jibge mata azurfa da zinariya,
waɗanda suka yi amfani wa Ba’al ba.

9 “Saboda haka zan ƙwace hatsina sa’ad da ya nuna,
da sabon ruwan inabina sa’ad da ya ƙosa.
Zan karɓe ulu nawa da lilina,
da take niyya ta rufe tsiraicinta.
10 Saboda haka yanzu zan buɗe tsiraicinta
a idanun kwartayenta;
ba wani da zai ƙwace ta daga hannuwana.
11 Zan tsayar da dukan bukukkuwarta,
bukukkuwarta na shekara-shekara, da kuma kiyaye bikin Sababbin Wata nata,
kwanakin Asabbacinta, dukan ƙayyadaddun bukukkuwarta.
12 Zan lalatar da inabinta da kuma itatuwan ɓaurenta,
waɗanda take cewa su ne abin da kwartayenta suka biya;
zan mayar da su kurmi,
namun jeji kuwa za su ci su.
13 Zan hukunta ta saboda kwanakin
da ta ƙone turare wa Ba’al;
ta yi wa kanta ado da zobai da duwatsu masu daraja,
ta bi kwartayenta,
amma ta manta da ni,”
in ji UBANGIJI.

14 “Saboda haka yanzu zan rarrashe ta;
zan bishe ta zuwa hamada
in kuma yi mata magana a hankali.
15 A can zan mayar mata da gonakin inabinta,
zan kuma sa Kwarin Akor* yă zama ƙofar bege.
A can za tă rera kamar a kwanakin ƙuruciyarta,
kamar a lokacin da ta fita daga Masar.

16 “A waccan rana,” in ji UBANGIJI,
“za ki ce da ni ‘mijina’;
ba za ki ƙara ce ni ‘maigidana’† ba.
17 Zan cire sunayen Ba’al daga leɓunanta;

* **2:15** Akor yana nufin wahala. † **2:16** miji, maigida. A Ibraniyanci kalman nan “maigida” daidai ne da sunan allahn nan Ba’al. Amma UBANGIJI ya yi alkawari cewa mutanensa za su kasance da zurfin dangantaka da shi (kamar mace da mijin masu aminci) a maimako bin abin da doka ta kafa kawai (kamar mata da “maigidanta”)

ba za a ƙara kira sunayensu ba.
18 A waccan rana zan yi alkawari dominsu
da namun jeji da kuma tsuntsayen sararin sama
da dukan halittu masu rarrafe a ƙasa.
Baka da takobi da yaƙi
zan sa su ƙare a ƙasar,
domin duk su zauna lafiya.
19 Zan ɗaura aure da ke har abada;
zan ɗaura aure da yake cikin adalci da gaskiya,
cikin ƙauna da jinƙai.
20 Zan ɗaura aure da yake cikin aminci
za ki kuwa yarda cewa ni ne UBANGIJI.

21 "A waccan rana zan amsa," in ji UBANGIJI,
"zan amsa wa sararin sama,
za su kuwa amsa wa ƙasa;
22 ƙasa kuma za tă amsa wa hatsi,
sabon ruwan inabi da kuma mai,
su kuma za su amsa wa Yezireyel.‡
23 Zan dasa ta wa kaina a ƙasar;
zan shuka ƙaunata ga wanda na ce 'Ba ƙaunatacciyata ba.'§
Zan faɗa wa waɗanda a ce 'Ba mutanena ba,*' 'Ku mutanena ne';
za su kuwa ce, 'Kai ne Allahna.' "

# 3

*Sulhun Hosiya da matarsa*

1 UBANGIJI ya ce mini, "Ka tafi, ka sāke nuna wa matarka ƙauna, ko da yake wani
yana son ta, ita kuma mazinaciya ce. Ka ƙaunace ta yadda UBANGIJI yake ƙaunar
Isra'ilawa, ko da yake sun juya ga waɗansu alloli suna kuma ƙauna wainar zabibi
mai tsarki."
2 Ta haka na saye ta da shekel goma sha biyar na azurfa da kuma wajen buhu na
sha'ir. 3 Sai na faɗa mata, "Za ki zauna tare* da ni kwanaki masu yawa; kada ki yi
karuwanci ko ki yi abuta da wani namiji, ni kuwa zan zauna tare† da ke."
4 Gama Isra'ilawa za su yi kwanaki masu yawa ba tare da sarki ko shugaba ba,
babu hadaya ko keɓaɓɓun duwatsu, babu efod ko gunki. 5 Daga baya Isra'ilawa za
su dawo su nemi UBANGIJI Allahnsu da kuma Dawuda sarkinsu. Za su je da rawan
jiki wajen UBANGIJI da kuma ga albarkunsa a kwanakin ƙarshe.

# 4

*Tuhuma a kan Isra'ila*

1 Ku ji maganar UBANGIJI, ku Isra'ilawa,
gama UBANGIJI yana da tuhumar da zai kawo
a kan ku waɗanda suke zama a ƙasar.
"Babu aminci, babu ƙauna,
babu yarda da Allah a cikin ƙasar.
2 Akwai la'ana ce kawai,* yin ƙarya da kisa,
yin sata da zina;
sun wuce gona da iri,

‡ **2:22** Yezireyel yana nufin shirye-shiryen Allah. § **2:23** Ibraniyanci Lo-Ruhama * **2:23** Ibraniyanci Lo-Ammi
* **3:3** Ko kuwa jira † **3:3** Ko kuwa jira * **4:2** Wato, a yi la'ana a kai

kisankai a kan kisankai.
3 Saboda wannan ƙasar tana makoki,†
kuma dukan waɗanda suke zama a cikinta sun lalace;
namun jeji da tsuntsayen sararin sama
da kuma kifin teku suna mutuwa.

4 “Amma kada wani mutum yă kawo tuhuma,
kada wani mutum yă zargi wani,
gama mutanenka suna kama da waɗanda
suke kawo tuhume-tuhume a kan firist ne.
5 Kuna tuntuɓe dare da rana,
annabawa ma suna tuntuɓe tare da ku.
Saboda haka zan hallaka mahaifiyarku,
6 mutanena suna hallaka saboda jahilci.

“Domin kun ƙi neman sani,
ni ma na ƙi ku a matsayin firistocina;
domin kun ƙyale dokar Allahnku,
ni ma zan ƙyale ’ya’yanku.
7 Yawan ƙaruwar firistoci,
haka suke yawan zunubi a kaina;
sun yi musaya Ɗaukakarsu da wani abin kunya.
8 Suna ciyar da kansu a kan zunuban mutanena
suna kuma haɗamar muguntarsu.
9 Zai kuwa zama, kamar yadda mutane suke, haka firistoci suke.
Zan hukunta dukansu saboda al’amuransu
in kuma sāka musu saboda ayyukansu.

10 “Za su ci amma ba za su ƙoshi ba;
za su shiga karuwanci amma ba za su ƙaru ba,
gama sun rabu da UBANGIJI
don su ba da kansu 11 ga karuwanci,
ga tsoho da kuma sabon ruwan inabi,
waɗanda suka ɗauke ganewar mutanena.
12 Sun nemi shawarar gunkin da aka yi da itace
suka kuwa sami amsa daga sanda.
Halin karuwanci yakan ɓad da su;
sun yi rashin aminci ga Allahnsu.
13 Suna miƙa hadaya a kan ƙwanƙolin duwatsu
suna kuma ƙone hadayu a kan tuddai,
a ƙarƙashin itatuwa oak, aduruku da katambiri,
inda inuwa take da daɗi.
Saboda haka ’ya’yanku mata suka juya wa karuwanci
surukanku mata kuma suka shiga yin zina.

14 “Ba zan hukunta ’ya’yanku mata
sa’ad da suka juya ga yin karuwanci ba,
balle surukanku mata,
sa’ad da suka yi zina,
gama mazan da kansu suna ma’amala da karuwai
suna kuma miƙa hadaya tare da karuwai na masujada,

† **4:3** Ko kuwa ta bushe

mutane marasa ganewa za su lalace!

15 “Ko da yake kun yi zina, ya Isra’ila,
kada Yahuda ya yi laifi.

“Kada ku tafi Gilgal;
kada ku haura zuwa Bet-Awen.‡
Kuma kada ku rantse cewa, ‘Muddin UBANGIJI yana a raye!’
16 Isra’ilawa masu taurinkai ne,
kamar karsana mai taurinkai.
Yaya UBANGIJI zai iya kiwonsu
kamar tumaki a makiyaya mai ɗanyar ciyawa?
17 Efraim ya haɗa kai da gumaka;
ku ƙyale shi kurum!
18 Ko ma sa’ad da abin shansu ya ƙare,
sai suka ci gaba da karuwancinsu;
masu mulkinsu suna ƙaunar abin kunya.
19 Guguwa za tă share su,
hadayunsu kuma za su jawo musu abin kunya.

# 5

*Hukunci a kan Isra’ila*

1 “Ku ji wannan, ku firistoci!
Ku kasa kunne, ku Isra’ilawa!
Ku saurara, ya ku gidan sarauta!
Wannan hukunci yana a kanku,
kun zama tarko a Mizfa,
ragar da aka shimfiɗa a kan Tabor.
2 ’Yan tawaye sun yi zurfi cikin kisan gilla.
Zan hore su duka.
3 Na san Efraim ƙaf;
Isra’ila ba a ɓoye take a gare ni ba.
Efraim, yanzu ka juya ka shiga karuwanci;
Isra’ila ta lalace.

4 “Ayyukansu ba su ba su dama
su koma ga Allahnsu ba.
Halin karuwanci yana cikin zuciyarsu;
ba su yarda da UBANGIJI ba.
5 Girmankan Isra’ila yana ba da shaida a kansu;
Isra’ilawa, har ma Efraim, sun yi tuntuɓe a cikin zunubinsu;
Yahuda ma ya yi tuntuɓe tare da su.
6 Sa’ad da suka tafi tare da garkunan shanu, tumaki da awakinsu
don su nemi UBANGIJI,
ba za su same shi ba;
ya janye kansa daga gare su.
7 Su marasa aminci ne ga UBANGIJI;
suna haihuwar shegu.
Yanzu bukukkuwar Sabon Watansu
za su cinye su da gonakinsu.

‡ **4:15** Bet-Awen yana nufin gidan mugunta (sunan Betel, wanda yake nufin gidan Allah).

8 “Amon kakaki a Gibeya,
ƙaho a Rama.
Ku yi kirarin yaƙi a Bet-Awen;
ku ja gaba, ya Benyamin.
9 Efraim za tă zama kango
a ranar hukunci.
A cikin kabilan Isra’ila
na yi shelar abin da yake tabbatacce.
10 Shugabannin Yahuda suna kamar waɗanda
suke matsar da duwatsun shaidar da aka sa a kan iyaka ne.
Zan zubo musu da fushina a kansu
kamar rigyawar ruwa.
11 An danne Efraim,
an murƙushe ta a shari’a
ta ƙudura ga bin gumaka.
12 Na zama kamar asu ga Efraim,
kamar ruɓa ga mutanen Yahuda.

13 “Sa’ad da Efraim ya ga ciwonsa,
Yahuda kuwa miyakunta,
sai Efraim ya juya ga Assuriya,
ya aika wurin babban sarki don neman taimako.
Amma bai iya warkar da kai ba,
bai iya warkar da miyakunka ba.
14 Gama zan zama kamar zaki ga Efraim,
kamar babban zaki ga Yahuda.
Zan yage su kucu-kucu in tafi;
zan kwashe su, ba wanda zai kuɓutar da su.
15 Sa’an nan zan koma wurina
sai sun yarda da laifinsu.
Za su kuma nemi fuskata;
cikin azabansu za su nace da nemana.”

# 6

### *Isra’ila marar tuba*

1 “Ku zo, mu koma ga UBANGIJI.
Ya yayyage mu kucu-kucu
amma zai warkar da mu;
ya ji mana ciwo
amma zai daure mana miyakunmu.
2 Bayan kwana biyu zai rayar da mu,
a rana ta uku zai tashe mu,
don mu rayu a gabansa.
3 Bari mu yarda da UBANGIJI;
bari mu nace gaba don mu yarda da shi.
Muddin rana tana fitowa,
zai bayyana;
zai zo mana kamar ruwan bazara,
kamar ruwan saman farko da yake jiƙe ƙasa.”

4 “Me zan yi da kai Efraim?
Me zan yi da kai Yahuda?

Kaunarku tana kamar hazon safiya,
kamar raɓar safiya da takan ɓace.
5 Saboda haka na yayyaga ku kucu-kucu tare da annabawana,
na kashe ku da kalmomin bakina;
hukuntaina sun haskaka kamar walƙiya a kanku.
6 Gama jinƙai nake bukata, ba hadaya ba,
ku kuma san Allah a maimakon hadayun ƙonawa.
7 Kamar Adamu, sun tā da alkawari,
sun yi mini rashin aminci a can.
8 Gileyad birni ce ta mugayen mutane,
da tabon alamun jini.
9 Kamar yadda mafasa sukan yi fakon mutum,
haka ƙungiyoyin firistoci suke;
suna kisa a hanya zuwa Shekem,
suna aikata laifofi bankunya.
10 Na ga wani abu mai bantsoro
a gidan Isra'ila.
A can Efraim ya miƙa wuya ga karuwanci
Isra'ila kuma ta ƙazantu.

11 "Ku kuma, ya mutanen Yahuda,
na shirya muku ranar girbi.

"A duk sa'ad da zan mayar da dukiya wa mutanena,

# 7

1 a duka sa'ad da zan warkar da Isra'ila,
zunuban Efraim za su tonu
za a kuma bayyana laifofin Samariya.
Suna ruɗu,
ɓarayi sukan fasa su shiga gidaje,
'yan fashi sukan yi fashi a tituna;
2 amma ba su gane
cewa na tuna da dukan ayyukan muguntarsu ba.
Zunubansu sun kewaye su;
kullum suna a gabana.

3 "Suna faranta wa sarki zuciya da muguntarsu,
shugabanni kuma da ƙarairayinsu.
4 Dukansu mazinata ne
suna ƙuna kamar matoya
wadda mai gashin burodi ba ya bukata yă tura mata wuta
daga cuɗe kullu har kumburinsa.
5 A ranar bikin sarkinmu
shugabanni sukan bugu da ruwan inabi,
yă yi cuɗanya da masu ba'a.
6 Zukatansu suna kamar matoya;
sukan kusace shi da wayo.
Muguwar aniyarsu takan yi ta ci dukan dare;
da safe sai ta ƙuna kamar harshen wuta.
7 Dukansu suna da zafi kamar matoya;
suna kashe masu mulkinsu.

Dukan sarakunansu sukan fāɗi,
kuma babu waninsu da yake kira gare ni.

8 “Efraim yana cuɗanya da al’ummai;
Efraim waina ne mai fāɗi da ba a juye ba.
9 Baƙi sun tsotse ƙarfinsa,
amma bai gane ba.
Gashi kansa ya cika da furfura,
amma bai lura ba.
10 Girmankan Isra’ila ya ba da shaida a kansa,
amma duk da haka
bai dawo ga Ubangiji Allahnsa
ko yă neme shi ba.

11 “Efraim yana kama da kurciya,
marar wayo, marar hankali,
yanzu yana kira ga Masar,
yanzu yana juyewa ga Assuriya.
12 Sa’ad da suka tafi, zan jefa ragata a kansu;
zai janye su ƙasa kamar tsuntsayen sararin sama.
Sa’ad da na ji suna tafiya tare,
zan kama su.
13 Kaitonsu,
domin sun kauce daga gare ni!
Hallaka za ta ă aukar musu,
domin sun tayar mini!
Na ƙudura in cece su
amma suna faɗar ƙarya a kaina.
14 Ba sa yin mini kuka da zuciyarsu
amma suna ihu a kan gadajensu.
Sukan taru wurin ɗaya don hatsi da ruwan inabi
amma su juya mini baya.
15 Na horar da su na kuma ƙarfafa su,
amma sun ƙulla mini maƙarƙashiya.
16 Ba sa juya ga Mafi Ɗaukaka;
suna kama da tanƙwararren baka.
Za a kashe shugabanninsu da takobi
saboda banzan maganganunsu.
Saboda wannan za a wulaƙanta su
a ƙasar Masar.

# 8

### *Isra’ila za tă girbe guguwa*

1 “Ka sa kakaki a leɓunanka!
Gaggafa tana a bisan gidan Ubangiji
domin mutane sun tā da alkawarina
suka kuma tayar wa dokata.
2 Isra’ila ta yi mini kuka,
‘Ya Allahnmu, mun yarda da kai!’
3 Amma Isra’ila sun ƙi abin da yake mai kyau;
abokin gāba zai fafare su.
4 Suna naɗa sarakuna, ba da izinina ba;

sun zaɓa shugabanni ba da yardanta ba.
Da azurfa da zinariya
sun ƙera gumaka wa kansu
wanda zai kai zuwa ga hallakarsu.
5 Ku zubar da gunkin maraƙinku, ya Samariya!
Fushina yana ƙuna a kansu.
Sai yaushe za su rabu da gumaka?
6 Su daga Isra'ila ne!
Wannan maraƙi, mai aikin hannu ne ya yi shi;
gunki ne ba Allah ba.
Za a farfashe shi kucu-kucu,
waccan maraƙin Samariya.

7 "Gama sun shuka iska
don haka za su girbe guguwa.
Hatsin da yake tsaye ba shi da kai,
ba zai yi tsaba ba.
Ko da ya yi tsaba ma,
baƙi ne za su ci.
8 An haɗiye Isra'ila;
yanzu tana cikin al'ummai
kamar abin da ba shi da amfani.
9 Gama sun haura zuwa Assuriya
kamar jakin jejin da yake yawo shi kaɗai.
Efraim ya sayar da kansa ga maza.
10 Ko da yake sun sayar da kansu a cikin al'ummai,
yanzu zan tattara su wuri ɗaya.
Za su fara lalacewa
a ƙarƙashi danniyar babban sarki.

11 "Ko da yake Efraim ya gina bagadai masu yawa don hadayun zunubi,
waɗannan sun zama bagade don yin zunubi.
12 Na rubuta musu abubuwa masu yawa na dokata,
amma suka ɗauke su tamƙar wani baƙon abu ne.
13 Suna miƙa hadayun da aka ba ni
su kuma ci nama,
amma UBANGIJI ba ya jin daɗinsu.
Yanzu zai tuna da muguntarsu
yă kuma hukunta zunubansu.
Za su koma Masar.
14 Isra'ila ya manta da Mahaliccinsa
ya kuma gina fadodi;
Yahuda ya gina katanga a yawancin garuruwansa.
Amma zan aiko da wuta a bisa biranensu
da zai cinye kagaransu."

# 9

*Hukunci domin Isra'ila*
1 Kada ku yi farin ciki, ya Isra'ila;
kada ku yi murna kamar waɗansu al'ummai.
Gama kun yi rashin aminci ga Allahnku;
kuna son hakkokin karuwa

a kowace masussuka.
2 Masussukai da wuraren matsin inabi ba za su ciyar da mutane ba;
sabon ruwan inabi zai kāsa musu.
3 Ba za su ci gaba da zama a ƙasar UBANGIJI ba;
Efraim zai koma Masar
yă kuma ci abinci marar tsarki a Assuriya.
4 Ba za su zuba hadayun ruwan inabi ga UBANGIJI ba,
ba kuwa hadayunsu za su gamshe shi ba.
Irin hadayun nan za su zama musu kamar burodin masu makoki;
duk wanda ya ci su zai ƙazantu.
Wannan abincin zai zama na kansu ne;
ba zai zo cikin haikalin UBANGIJI ba.

5 Me za ku yi a ƙayyadaddiyar ranar bukukkuwarku,
a ranakun bikin UBANGIJI?
6 Ko da sun kuɓuta daga hallaka,
Masar za tă tattara su,
Memfis kuma za tă binne su.
Sarƙaƙƙiya za tă mamaye kayan azurfansu,
ƙayayyuwa su tsiro a cikin tentunansu.
7 Kwanakin hukunci suna zuwa,
kwanakin ba da lissafi suna a kusa.
Bari Isra'ila su san da wannan.
Saboda zunubanku sun yi yawa
ƙiyayyarku kuma ta yi yawa,
har ake ɗauka annabi wawa ne,
mutumin da aka iza kuwa mahaukaci.
8 Annabi, tare da Allahna,
su ne masu tsaro a bisa Efraim,*
duk da haka tarko na jiransa a dukan hanyoyi,
da kuma ƙiyayya a cikin gidan Allahnsa.
9 Sun nutse da zurfi cikin lalaci,
kamar a kwanakin Gibeya.
Allah zai tuna da muguntarsu
yă kuma hukunta su saboda zunubansu.

10 "Sa'ad da na sami Isra'ila,
ya zama kamar samun inabi a hamada;
sa'ad da na ga kakanninku,
ya zama kamar ganin 'ya'yan itace na farko a itacen ɓaure.
Amma sa'ad da suka zo Ba'al-Feyor,
suka keɓe kansu wa gumaka bankunya
sai suka zama abubuwan banƙyama kamar abubuwan da suke ƙauna.
11 Darajar Efraim za tă yi firiya tă tafi kamar tsuntsu,
ba haihuwa, ba juna biyu, ba ɗaukar ciki.
12 Ko da sun yi renon 'ya'ya,
zan sa su yi baƙin cikin kowannensu.
Kaitonsu
sa'ad da na juya musu baya!
13 Na ga Efraim, kamar birnin Taya,
da aka kafa a wuri mai daɗi.

* **9:8** Ko kuwa Annabi ne mai tsaro a bisa Efraim, mutanen Allahna

Amma Efraim zai fitar
da ʼyaʼyansu ga masu yanka.”

14 Ka ba su, ya UBANGIJI
Me za ka ba su?
Ka ba su mahaifar da za su yi ɓarin ciki
da busassun nono.

15 “Saboda dukan muguntarsu a Gilgal,
na ƙi su a can.
Saboda ayyukansu na zunubi,
zan kore su daga gidana.
Ba zan ƙara ƙaunace su ba;
dukan shugabanninsu ʼyan tawaye ne.
16 An ka da Efraim,
saiwarsu ta bushe,
ba sa ba da amfani.
Ko da sun haifi ʼyaʼya
zan kashe waɗanda suka fi ƙauna.”

17 Allahna zai ƙi su
saboda ba su yi masa biyayya ba;
za su zama masu yawo a cikin alʼummai.

# 10

1 Israʼila kuringa ce mai yaɗuwa;
ya fitar da ʼyaʼya wa kansa.
Yayinda ʼyaʼyan suka ƙaru,
ya gina ƙarin bagadai;
da ƙasarsa ta wadata,
ya yi wa keɓaɓɓun duwatsu ado.
2 Zuciyarsu masu ruɗu ne,
yanzu kuwa dole su ɗauki laifinsu.
UBANGIJI zai rushe bagadansu
yǎ kuma hallaka keɓaɓɓun duwatsunsu.

3 Saʼan nan za su ce, “Ba mu da sarki
domin ba mu girmama UBANGIJI ba.
Amma ko da ma muna da sarki,
me zai yi mana?”
4 Sun yi alkawura masu yawa,
suka yi rantsuwar ƙarya
da kuma yarjejjeniyoyi;
saboda haka ƙararraki suka taso
kamar ciyayi masu dafi da aka nome a gona.
5 Mutanen da suke zama a Samariya suna tsoro
saboda gunki maraƙin Bet-Awen.*
Mutanensa za su yi makokinsa,
haka ma firistocinsa matsafa,
waɗanda suka yi farin ciki a kan darajarsa,

* **10:5** Bet-Awen yana nufin gidan mugunta (suna don Betel, wanda yake nufin gidan Allah).

don an ɗauke ta daga gare su aka kai ta zaman bauta.
6 Za a ɗauke shi a kai Assuriya
kamar gandu wa babban sarki.
Efraim zai sha kunya;
Isra'ila zai sha kunya saboda gumakan itacensa.
7 Samariya da sarkinta za su ɓace
kamar kumfa a bisa ruwaye.
8 Za a hallaka masujadai kan tudu na mugunta
zunubin Isra'ila ne.
Kayayuwa da sarƙaƙƙiya za su yi girma
su rufe bagadansu.
Sa'an nan za su ce wa duwatsu, "Ku rufe mu!"
Ga tuddai kuma, "Ku fāɗo a kanmu!"

9 "Tun daga kwanakin Gibeya, kun yi zunubi, ya Isra'ila,
a can kuwa kuka ci gaba.†
Yaƙi bai cimma
masu aikata mugunta a Gibeya ba?
10 Sa'ad da na ga dama, zan hukunta su;
al'ummai za su taru su yi gāba da su
don su daure su saboda zunubansu da suka riɓanya.
11 Efraim horarriyar karsana ce
mai son sussuka;
saboda haka zan sa karkiya
a kyakkyawan wuyanta.
Zan bi da Efraim,
Dole Yahuda yă yi noma,
dole kuma Yaƙub yă ja garman noma.
12 Ku shuka wa kanku adalci,
ku girbe 'ya'yan jinƙai marar ƙarewa,
ku kuma nome ƙasar da ba a nome ba;
gama lokaci ne na neman Ubangiji,
sai ya zo
ya zubo adalci a kanku.
13 Amma kun shuka mugunta,
kuka girbe mugu
kuka ci 'ya'yan ruɗu.
Domin kun dogara da ƙarfinku
da kuma a jarumawanku masu yawa,
14 hayaniyar yaƙi za tă tashi gāba da mutanenku,
saboda a ragargaza kagaranku,
kamar yadda Shalman ya ragargaza Bet-Arbel a ranar yaƙi,
sa'ad da aka fyaɗa uwaye tare da 'ya'yansu da ƙasa.
15 Haka zai faru da kai, ya Betel,
domin muguntarka ta yi yawa.
Sa'ad da wannan rana ta zo,
za a hallaka sarkin Isra'ila ƙaƙaf.

# 11

*Kaunar Allah domin Isra'ila*

† **10:9** Ko kuwa a can aka ɗauki matsayi

1 “Sa’ad da Isra’ila yake yaro, na ƙaunace shi,
daga Masar kuma na kira ɗana.
2 Amma yawan kiran da na yi wa Isra’ila
haka nesa da ni da suke ta yi.
Suka miƙa hadaya ga Ba’al
suka kuma ƙona turare ga siffofi.
3 Ni ne na koya wa Efraim tafiya
ina kama su da hannu;
amma ba su gane
cewa ni ne na warkar da su ba.
4 Na bishe su da linzamin alheri da tausayi,
da ragamar ƙauna;
Na cire karkiya daga wuyansu
na kuma rusuna na ciyar da su.

5 “Ba za su koma Masar ba
Assuriya kuma ba za tă yi mulki a bisansu ba
saboda sun ƙi su tuba ba?
6 Takuba za su yi ta wulgawa a biranensu,
za su hallaka sandunan ƙarafan ƙofofinsu
su kuma kawo ƙarshen ƙulle-ƙullensu.
7 Mutanena sun ƙudura su juye daga gare ni.
Ko da ma suka yi kira ga Mafi Ɗaukaka,
ta ko ƙaƙa ba zai girmama su ba.

8 “Yaya zan ba da kai, Efraim?
Yaya zan miƙa ka, Isra’ila?
Yaya zan yi da kai kamar Adma?
Yaya zan yi da kai kamar Zeboyim?
Zuciyata ta canja a cikina;
dukan tausayina ya huru.
9 Ba zan zartar da fushina mai zafi ba,
ba kuwa zan juya in ragargaza Efraim ba.
Gama ni Allah ne, ba mutum ba,
Mai Tsarki a cikinku.
Ba zan zo cikin fushi ba.
10 Za su bi UBANGIJI;
zai yi ruri kamar zaki.
Sa’ad da ya yi ruri,
’ya’yansa za su zo da rawan jiki daga yamma.
11 Za su zo da rawan jiki
kamar tsuntsaye daga Masar,
kamar kurciyoyi daga Assuriya.
Zan zaunar da su a cikin gidajensu,”
in ji UBANGIJI.

### *Zunubin Isra’ila*

12 Mutanen Efraim sun kewaye ni da ƙarairayi,
gidan Isra’ila da ruɗu.
Mutanen Yahuda kuma suna yi wa Allah ƙin ji,
har ma a kan Mai Tsarkin nan mai aminci.

# 12

1 Efraim yana kiwo a kan iska;
yana fafarar iskar gabas dukan yini
yana riɓaɓɓanya ƙarairayi da rikici.
Ya yi yarjejjeniya da Assuriya
ya kuma aika wa Masar man zaitun.
2 UBANGIJI yana da ƙarar da zai kawo a kan Yahuda;
zai hukunta Yaƙub bisa ga hanyoyinsa
zai sāka masa bisa ga ayyukansa.
3 A cikin mahaifa ya cafke ɗiɗɗigen ɗan'uwansa;
a matsayin mutum ya yi kokawa da Allah.
4 Ya yi kokawa da mala'ika ya kuma rinjaye shi;
ya yi kuka ya kuma yi roƙo don tagomashi.
Ya same shi a Betel
ya kuma yi magana da shi a can,
5 UBANGIJI Allah Maɗaukaki,
UBANGIJI ne sunansa sananne!
6 Amma dole ku koma ga Allahnku;
ku ci gaba da ƙauna da yin gaskiya,
ku kuma saurari Allahnku kullum.

7 Ɗan kasuwa yana amfani da mudu marar gaskiya;
yana jin daɗin cuta.
8 Efraim yana fariya yana cewa,
"Ni mai arziki ne ƙwarai; na azurta.
Da dukan wadatata ba za a sami
wani laifi ko zunubi a gare ni ba."

9 "Ni ne UBANGIJI Allahnku,
wanda ya fitar da ku daga* Masar;
zan sa ku sāke zauna a tentuna,
kamar a kwanakin ƙayyadaddun bukukkuwanku.
10 Na yi magana da annabawa,
na ba su wahayi da yawa
na kuma ba da misalai ta wurinsu."

11 Gileyad mugu ne?
Mutanensa mutanen banza ne!
Suna miƙa bijimai a Gilgal?
Bagadansu za su zama tsibin duwatsu.
A gonar da aka nome.
12 Yaƙub ya gudu zuwa ƙasar Aram;†
Isra'ila ya yi bauta don yă sami mata,
domin kuma yă biya, sai da ya yi kiwon tumaki.
13 UBANGIJI ya yi amfani da annabi don yă fitar da Isra'ila daga Masar
ta wurin annabi ya lura da shi.
14 Amma Efraim ya yi muguwar tsokana da ta sa ya yi fushi;
shugabansa zai ɗora musu hakkin jini a kansa
kuma zai sāka masa saboda wulaƙancinsa.

* 12:9 Ko kuwa Allah / tun kuna cikin † 12:12 Wato, Arewa maso yamma Mesofotamiya

# 13

*Fushin Ubangiji a kan Isra'ila*

1 Sa'ad da Efraim ya yi magana, mutane sun yi rawan jiki;
an girmama shi a cikin Isra'ila.
Amma sai ya zama mai laifi na yin wa Ba'al sujada, ya kuwa mutu.
2 Yanzu sai yin zunubi a kai a kai suke;
suna yin gumaka wa kansu daga azurfansu,
da wayo suna sarrafa siffofi,
dukansu aikin masu aikin hannu ne.
Ana magana waɗannan mutane cewa,
"Suna miƙa hadayar mutum
su kuma sumbaci* gumakan maruƙa."
3 Saboda haka za su zama kamar hazon safiya,
kamar raɓar safen da yakan kakkaɓe,
kamar ƙaiƙayin da ake tankaɗe daga masussuka,
kamar hayaƙin da yake fita daga taga.

4 "Amma ni ne Ubangiji Allahnku,
wanda ya fitar da ku daga Masar.
Ba za ku yarda da wani Allah ba sai ni,
ba wani Mai Ceto in ban da ni.
5 Na lura da ku a hamada,
cikin ƙasar mai ƙunar zafi.
6 Sa'ad da na ciyar da su sun ƙoshi;
sa'ad da suka ƙoshi, sai suka fara taƙama;
sai suka manta da ni.
7 Saboda haka zan hau kansu kamar zaki,
zan ɓuya a bakin hanya kamar damisa.
8 Kamar beyar da aka ƙwace mata 'ya'yanta,
zan fāɗa musu in ɓarke su.
Kamar zaki zan cinye su;
kamar naman jeji zan yayyage su.

9 "An hallaka ku, ya Isra'ila,
domin kun tayar mini, kun tayar wa mai taimakonku.
10 Ina sarkinku, da zai cece ku?
Ina masu mulkinku cikin dukan garuruwanku,
waɗanda kuka ce,
'Ba mu sarki da shugabanni'?
11 Saboda haka cikin fushina na ba ku sarki,
kuma cikin hasalata na ɗauke shi.
12 An yi ajiyar laifin Efraim,
aka lissafta zunubansa.
13 Naƙuda ta zo masa kamar a mace mai haihuwa,
amma shi yaro ne marar hikima;
sa'ad da lokaci ya kai,
ba ya zuwa inda mahaifa ta buɗe.

14 "Zan fanshe su daga ikon kabari;
zan cece su daga mutuwa.

* **13:2** Ko kuwa "Mutanen da suke hadaya / sumbaci"

Ina annobanki, ya mutuwa?
Ina hallakarka, ya kabari?

“Ba zan ji tausayi ba,
15 ko da ma ya ci gaba cikin ’yan’uwansa.
Iskar gabas daga UBANGIJI za tă zo,
tana hurawa daga hamada;
maɓulɓularsa za tă kafe
rijiyarsa kuma ta bushe.
Za a kwashi kaya masu daraja
na ɗakin ajiyarsa ganima.
16 Dole mutanen Samariya su ɗauki laifinsu,
domin sun tayar wa Allahnsu.
Za a kashe su da takobi;
za a fyaɗa ƙananansu da ƙasa,
za a ɓarke matansu masu ciki.”

## 14

*Tuba don kawo albarka*

1 Ku dawo, ya Isra’ila, ga UBANGIJI Allahnku.
Zunubanku ne sun zama sanadin fāɗuwarku!
2 Ku ɗauki magana tare da ku
ku komo wurin UBANGIJI.
Ku ce masa,
“Ka gafarta mana dukan zunubanmu
ka kuma karɓe mu da alheri,
don mu iya yabe ka da leɓunanmu.*
3 Assuriya ba za su iya cece mu ba;
ba za mu hau dawakan yaƙi ba.
Ba za mu ƙara ce, ‘Allolinmu’
wa abin da hannuwanmu suka yi ba,
gama a gare ka ne maraya yakan sami jinƙai.”

4 “Zan gyara ɓatancinsu
in kuma ƙaunace su a sake,
gama fushina ya juya daga gare su.
5 Zan zama kamar raɓa ga Isra’ila
zai yi fure kamar lili.
Kamar al’ul na Lebanon
zai sa saiwarsa zuwa ƙasa;
6 tohonsa za su yi girma.
Darajarsa za tă zama kamar itacen zaitun,
ƙanshinsa kamar al’ul na Lebanon.
7 Mutane za su sāke zauna a inuwarsa.
Zai haɓaka kamar ƙwayar hatsi.
Zai yi fure kamar kuringa,
zai zama sananne kamar ruwan inabi daga Lebanon.
8 Efraim zai ce, me kuma zai haɗa ni da gumaka?
Zan amsa masa in kuma lura da shi.
Ni kamar koren itacen fir ne;
amincinka yana fitowa daga gare ni ne.”

* **14:2** Ko kuwa miƙa leɓunanmu kamar hadayun bijimai

9 Wane ne yake da hikima? Zai gane waɗannan abubuwa.
Hanyoyin UBANGIJI daidai ne;
masu adalci sukan yi tafiya a kansu,
amma ʼyan tawaye sukan yi tuntuɓe a kansu.

# Yowel

1 Maganar UBANGIJI wadda ta zo wurin Yowel ɗan Fetuwel.

*Mamayar da fāra ta yi*

2 Ku ji wannan, ku dattawa,
ku kasa kunne, dukan waɗanda suke zaune a ƙasar.
Ko wani abu makamancin haka ya taɓa faruwa a kwanakinku
ko a kwanakin kakanninku?
3 Ku faɗa wa ’ya’yanku,
bari kuma ’ya’yanku su faɗa wa ’ya’yansu,
’ya’yansu kuma su faɗa wa tsara ta gaba.
4 Abin da ɗango ya bari
fāri masu girma sun cinye;
abin da fāri masu girma suka bari,
burduduwa ta cinye;
abin da burduduwa ta bari sauran kwari* sun cinye.

5 Ku farka, ku bugaggu, ku yi kuka!
Ku yi kuka da ƙarfi, ku dukan mashayan ruwan inabi;
ku yi kuka mai ƙarfi saboda sabon ruwan inabi,
gama an riga an ƙwace ta daga leɓunanku.
6 Wata al’umma ta mamaye ƙasata,
tana da ƙarfi ba ta kuma ƙidayuwa;
tana da haƙoran zaki,
da zagar zakanya.
7 Ta mayar da kuringar inabina kango
ta kuma lalatar da itatuwan ɓaurena.
Ta ɓamɓare bayansu duka
ta kuma jefar da su
ta bar rassansu fari fat.

8 Ku yi makoki kamar budurwa†
a cikin tsummoki
tana baƙin ciki domin mijinta‡ na ƙuruciyarta.
9 Hadayun hatsi da hadayun sha
an yanke su daga gidan UBANGIJI.
Firistoci suna makoki,
su waɗanda suke yi wa UBANGIJI hidima.
10 Filaye sun zama marasa amfani,
ƙasa ta bushe;§
an lalatar da hatsi,
sabon ruwan inabin ya bushe,
mai kuma ba amfani.

11 Ku fid da zuciya, ku manoma,

* **1:4** A nan ma’anar kalmomin nan huɗu na Ibraniyanci da aka yi amfani da su da yake nuna fāra ba a san tabbatacciyar ma’anar ba. † **1:8** Ko kuwa yarinya ‡ **1:8** Ko kuwa wanda suka yi alkawarin aure § **1:10** Ko kuwa ƙasa tana makoki

ku yi ihu, ku masu noma inabi;
ku yi baƙin ciki saboda alkama da sha'ir,
saboda an lalata girbin filaye.
12 Kuringar inabin ta bushe
itacen ɓaure kuma ya yi yaushi,
'ya'yan rumman, itacen dabino da itacen gawasa,
dukan itatuwan filaye, sun bushe.
Tabbatacce farin cikin 'yan adam
ya bushe.

*Kira don makoki*

13 Ku sa tsummoki, ya firistoci, ku yi makoki;
ku yi ihu, ku da kuke yin hidima a gaban bagade.
Zo, ku kwana saye da tsummoki,
ku waɗanda kuke yi wa Allahna hidima,
gama an yanke hadayun hatsi da hadayun sha
daga gidan Allahnku.
14 Ku yi shelar azumi mai tsarki;
ku kira tsarkakan taro.
Ku kira dattawa
da kuma dukan mazaunan ƙasar
zuwa gidan UBANGIJI Allahnku,
ku kuma yi kuka ga UBANGIJI.

15 Kaito saboda wannan rana!
Gama ranar UBANGIJI ta kusa,
za tă zo kamar hallaka daga wurin Maɗaukaki.*

16 Ba a yanke abinci
a idanunmu,
farin ciki da kuma murna
daga gidan Allahnmu ba?
17 Iri suna ta yanƙwanewa
a busasshiyar ƙasa†
Ɗakunan ajiya sun lalace,
an rurrushe rumbunan hatsin,
gama hatsi ya ƙare.
18 Ji yadda dabbobi suke nishi!
Garkunan shanu sun ruɗe
saboda ba su da ciyawa,
har garkunan tumaki ma suna shan wahala.

19 A gare ka, ya UBANGIJI, nake kira,
gama wuta ta cinye wurin kiwo
harshen wuta kuma ya ƙone dukan itatuwan jeji.
20 Har ma namun jeji suna haki gare ka;
rafuffuka sun bushe
wuta kuma ta cinye wurin kiwo a jeji.

---

* **1:15** Da Ibraniyanci Shaddai † **1:17** ma'anar wannan kalma da Ibraniyanci ba ta da tabbas.

# 2

*Rundunar fāra*

1 Ku busa ƙaho a cikin Sihiyona;
ku yi karar amo a tsaunina mai tsarki.

Bari dukan mazaunan ƙasar su yi rawan jiki,
gama ranar UBANGIJI tana zuwa.
Tana gab da faruwa
2 rana ce ta baƙin duhu ƙirin,
ranar gizagizai ce baƙi ƙirin.
Babbar rundunar mayaƙa mai ƙarfi tana zuwa
kamar ketowar alfijir a kan duwatsu
yadda ba a taɓa ganin irinta ba,
ba kuwa za a ƙara ganin irinta ba har tsararraki masu zuwa.

3 A gabansu wuta tana ci,
a bayansu ga harshen wuta yana ci,
A gabansu ƙasa ta yi kamar gonar Eden,
a bayansu kuma jeji ne wofi,
babu abin da ya kuɓuce musu.
4 Suna da kamannin dawakai;
suna gudu kamar dokin yaƙi.
5 Da motsi kamar na kekunan yaƙi
sun tsallake ƙwanƙolin duwatsu,
kamar ƙarar harshen wuta mai cin tattaka,
kamar runduna mai ƙarfi wadda ta ja dāgār yaƙi.

6 Da ganinsu, al'ummai sun kamu da azaba;
kowace fuska ta yanƙwane.
7 Sukan auka kamar jarumawa;
sukan hau katanga kamar sojoji.
Kowa yana takawa bisa ga tsari,
ba mai kaucewa.
8 Ba sa turin juna,
kowane yakan miƙe gaba.
Sukan kutsa cikin abokan gāba
ba mai tsai da su.
9 Sukan ruga cikin birni,
suna gudu a kan katanga.
Sukan hau gidaje,
sukan shiga ta tagogi kamar ɓarayi.

10 A gabansu duniya takan girgiza,
sararin sama kuma yakan jijjigu,
rana da wata su yi duhu,
taurari kuma ba sa ba da haske.
11 UBANGIJI ya yi tsawa
wa shugaban mayaƙansa;
sojojinsa sun fi a ƙirge
masu ƙarfi ne kuma su waɗanda suke biyayya da umarninsa.
Ranar UBANGIJI da girma take;

mai banrazana.
Wa zai iya jure mata?

*Ku kyakkece zuciyarku*

12 "Ko yanzu", in ji UBANGIJI,
"Ku juyo gare ni da dukan zuciyarku,
da azumi da kuka da makoki."

13 Ku kyakkece zuciyarku
ba rigunanku ba.
Ku juyo ga UBANGIJI Allahnku,
gama shi mai alheri ne mai tausayi kuma
mai jinkirin fushi da yawan ƙauna,
yakan kuma janye daga aika da bala'i.
14 Wa ya sani? Ko zai juya yă kuma ji tausayi
yă sa mana albarka
ta wurin hadaya ta gari da hadaya ta sha
wa UBANGIJI Allahnku.

15 A busa ƙaho a Sihiyona,
a yi shelar azumi mai tsarki,
a kira tsarkakan taro.
16 A tattara mutane;
ku tsarkake taron;
ku kawo dattawa wuri ɗaya;
ku kuma tara yara,
da waɗanda suke shan mama.
Bari ango yă bar ɗakinsa
amarya kuma lolokinta.
17 Bari firistocin da suke yin hidima a gaban UBANGIJI,
su yi kuka tsakanin filin haikali da bagade.
Bari su ce, "Ka cece mutanenka, ya UBANGIJI.
Kada ka bar gādonka yă zama abin dariya,
da abin ba'a a cikin al'ummai.
Me zai sa a ce a cikin mutane, 'Ina Allahnsu yake?' "

*Amsar UBANGIJI*

18 Ta haka UBANGIJI zai yi kishin ƙasarsa
yă kuma ji tausayin mutanensa.
19 UBANGIJI zai amsa* musu ya ce,
"Ina aika da hatsi, sabon ruwan inabi, da mai,
isashe da zai ƙosar da ku sosai;
ba kuma zan ƙara maishe ku
abin dariya ga al'ummai ba.

20 "Zan kori sojojin arewa nesa da ku,
in tura su cikin busasshiyar ƙasa marar amfani kuma,
kuma da sawunsu na gaba zan tura su zuwa gabashin teku†
da kuma sawunsu na baya tura su zuwa yammanci a Bahar Rum.‡
Warinsu kuma zai bazu;
ɗoyinsu zai tashi."

* **2:19** Ko kuwa UBANGIJI yă ji kishin / da kuma tausayawa / 19 UBANGIJI ya amsa † **2:20** Wato, Mediterraniyan.
‡ **2:20** wannan teku na Bahar Maliya ne

Tabbatacce ya yi al’amura masu girma.§
21 Kada ki ji tsoro, ya ƙasa;
ki yi murna ki kuma yi farin ciki.
Tabbatacce UBANGIJI ya yi abubuwa masu girma.
22 Kada ku ji tsoro, ya ku namun jeji,
gama wuraren kiwo sun yi kore shar.
Itatuwa suna ba da ’ya’yansu;
itacen ɓaure da na inabi suna ba da amfaninsu.
23 Ku yi murna, ya ku mutanen Sihiyona,
ku yi farin ciki cikin UBANGIJI Allahnku,
gama ya ba ku
ruwan bazara cikin adalci.*
Yakan aika muku yayyafi a yalwace,
na bazara da na kaka, kamar dā.
24 Masussukai za su cika da hatsi;
randuna za su cika da sabon ruwan inabi da mai suna zuba.

25 “Zan mayar muku da abin da fāra suka ci a waɗannan shekaru
waɗanda ɗango da fāra masu gaigayewa,
da kuma sauran fāra da tarin fāra†
babban mayaƙan da na aika don su fāɗa muku.
26 Za ku sami a wadace ku ci, har sai kun ƙoshi,
za ku kuma yabi sunan UBANGIJI Allahnku,
wanda ya yi muku ayyukan banmamaki;
mutanena ba za su ƙara shan kunya ba.
27 Sa’an nan za ku sani ina cikin Isra’ila,
cewa ni ne UBANGIJI Allahnku,
babu wani kuma;
mutanena ba za su ƙara shan kunya ba.

### *Ranar UBANGIJI*

28 “Daga baya kuma,
zan zuba Ruhuna a bisan dukan mutane.
’Ya’yanku maza da mata za su yi annabci,
tsofaffinku za su yi mafarkai,
matasanku za su ga wahayoyi.
29 Har ma a bisan bayina, maza da mata,
zan zuba Ruhuna a kwanakin nan.
30 Zan nuna abubuwan banmamaki a cikin sammai
da kuma a kan duniya,
za a ga jini da wuta da murtukewar hayaƙi.
31 Rana za tă duhunta
wata kuma yă zama jini
kafin isowar babbar ranan nan mai banrazana ta UBANGIJI.
32 Amma dukan waɗanda suka nemi
UBANGIJI za su tsira.
Kamar yadda UBANGIJI ya ce,
gama a Dutsen Sihiyona da Urushalima
akwai ceto,
a cikin waɗannan da UBANGIJI ya kira.

---

§ **2:20** Ko kuwa ya tashi. Tabbatacce ya yi abubuwa masu girma * **2:23** ko / mai koyar da gaskiya † **2:25** Takamamme ma’anar kalmomin nan guda huɗu na Ibraniyancin da aka yi amfani da su a nan domin fāra babu wanda ya sani.

# 3

*An shari'anta al'ummai*

1 "A waɗancan kwanaki da kuma a wancan lokaci,
sa'ad da zan maido da arzikin Yahuda da Urushalima,
2 zan tattara dukan al'ummai
in kuma kawo su Kwarin Yehoshafat*
Can zan yi musu shari'a
game da gādona, mutanena Isra'ila,
gama sun warwatsar da mutanena a cikin al'ummai
sun kuma raba ƙasata.
3 Sun jefa ƙuri'a a kan mutanena
suna kuma sayar da yara maza don karuwanci,
sun sayar da 'yan matan domin ruwan inabi
wanda za su sha.

4 "Yanzu mene ne damuwarku da ni, ya Taya da Sidon da kuma dukan mazaunan
yankunan Filistiya? Kuna ƙoƙari ku sāka mini don abin da na yi ne? In kuna sāka
mini ne, to, da gaggawa zan mayar muku da sakayya a kanku. 5 Gama kun kwashe
azurfata da zinariyata kun kuma washe dukiyata mafi kyau kun kai cikin haikalinku.
6 Kun sayar da mutanen Yahuda da na Urushalima ga mutanen Hellenawa, don ku
aika da su nesa da ƙasarsu.

7 "Duba, zan dawo da su daga wuraren da kuka sayar da su, in kuma yi muku
abin da kuka yi musu. 8 Zan sayar da 'ya'yanku maza da mata ga mutanen Yahuda,
su kuma za su sayar da su ga mutanen Sabenawa, al'umma da take nesa da ku."
UBANGIJI ya faɗa.

9 Ku yi shelar wannan ga al'ummai.
Ku yi shirin yaƙi!
Ku tā da jarumawa!
Bari mayaƙa su ja kusa su kai hari.
10 Ku bubbuge garemaninku su zama takuba
da kuma laujenku su zama māsu.
Bari raunana su ce,
"Ni mai ƙarfi ne!"
11 Ku gaggauta, dukanku al'ummai daga kowane ɓangare,
ku tattaru a can.

Ka sauko da mayaƙanka, ya UBANGIJI!

12 "Bari a tā da dukan al'ummai;
bari su kutsa zuwa Kwarin Yehoshafat
gama a can zan zauna
in shari'anta dukan al'ummai daga kowane ɓangare.
13 Ku fito da lauje,
gama girbi ya nuna.
Ku zo, ku tattaka inabin,
gama wurin matsewar ruwan inabi ya cika
randunan tarawa kuma sun cika har suna zuba,
muguntarsu da girma take!"

14 Dubun dubbai
suna a cikin kwarin yanke shawara!
Gama ranar UBANGIJI ta yi kusa

---

* **3:2** Yehoshafat yana nufin UBANGIJI ya shari'anta; haka ma a aya 12.

a cikin kwarin yanke shawara.
15 Za a duhunta rana da wata,
taurari kuma ba za su ba da haske ba.
16 UBANGIJI zai yi ruri daga Sihiyona
tsawa kuma daga Urushalima;
duniya da sararin sama za su yi rawan jiki.
Amma UBANGIJI zai zama mafakar mutanensa,
mafaka ga mutanensa Isra'ila.

### *Albarka domin mutanen Allah*

17 "Sa'an nan za ku san cewa ni, UBANGIJI Allahnku,
ina zaune a Sihiyona, dutsena mai tsarki.
Urushalima za tă zama mai tsarki;
baƙi ba za su ƙara mamaye ta ba.

18 "A wannan rana duwatsu za su ɗiga da sabon ruwan inabi,
tuddai kuma za su malmalo madara;
dukan rafuffukan Yahuda za su yi ta gudano da ruwa.
Maɓulɓula kuma za tă fito daga gidan UBANGIJI
haka ma ruwa a kwarin itatuwan ƙirya.†
19 Amma Masar za tă zama kango,
Edom kuma hamada marar amfani,
saboda kama-karyar da aka yi wa mutanen Yahuda,
a ƙasar da aka zub da jinin marasa laifi.
20 Za a zauna a Yahuda har abada
Urushalima kuma daga tsara zuwa tsara.
21 Alhakin jininsu, wanda ban gafarta ba,
zan gafarta."

UBANGIJI yana zama a Sihiyona!

† **3:18** Ko kuwa kwarin Shittim

# Amos

[1] Kalmomin Amos, ɗaya daga cikin makiyayan Tekowa, abubuwan da ya gani game
da Isra'ila shekaru biyu kafin a yi girgizar ƙasa, a lokacin da Uzziya yake sarkin
Yahuda, Yerobowam ɗan Yowash kuma yake sarkin Isra'ila.

[2] Ya ce,
"UBANGIJI ya yi ruri daga Sihiyona
ya kuma yi tsawa daga Urushalima;
wuraren kiwo duk sun bushe,
dutsen Karmel kuma ya yi yaushi."

*Hukunci a kan maƙwabtan Isra'ila*

[3] Ga abin da UBANGIJI ya ce,
"Saboda zunubai uku na Damaskus,
har guda huɗu ma, ba zan fasa hukunta su ba.
Domin sun ci zalunci Gileyad
zalunci mai tsanani,
[4] zan sa wuta a gidan Hazayel,
da za tă ƙona kagarun Ben-Hadad.
[5] Zan kakkarye ƙofofin Bet-Damaskus;
zan hallaka sarkin da yake cikin* Kwarin Awen†
da kuma mai riƙe da sandar mulkin Bet-Eden.
Mutanen Aram za su je bauta a ƙasar Kir,"
in ji UBANGIJI.
[6] Ga abin da UBANGIJI ya ce,
"Saboda zunubai uku na Gaza,
har guda huɗu ma, ba zan fasa hukunta su ba.
Don sun kwashe al'umma gaba ɗaya
sun sayar wa Edom,
[7] Zan aika da wuta a katangar Gaza
ta ƙone duk kagarunta.
[8] Zan hallaka sarkin‡ Ashdod
da kuma mai riƙe da sandar mulki na Ashkelon.
Zan hukunta Ekron,
har sai dukan Filistiyawa sun mutu,"
in ji UBANGIJI Mai Iko Duka.
[9] Ga abin da UBANGIJI ya ce,
"Saboda zunubai uku na Taya,
har guda huɗu ma, ba zan fasa hukunta su ba.
Don sun kwashe al'umma gaba ɗaya sun kai su bauta a Edom,
ba su kula da yarjejjeniyar da aka yi ta zama kamar 'yan'uwa ba,
[10] zan aika da wuta a Taya,
da za tă ƙone kagarunta."
[11] Ga abin da UBANGIJI ya ce,
"Saboda zunubai uku na Edom,
har guda huɗu ma, ba zan fasa hukunta shi ba.
Don ya fafari ɗan'uwansa da takobi,

* **1:5** Ko kuwa mazaunan † **1:5** Awen yana nufin mugunta. ‡ **1:8** Ko kuwa mazaunan

babu tausayi,
domin ya ci gaba da fusata
bai yarda yă huce daga fushinsa ba.
12 Zan aika wuta a Teman
da za tă ƙone kagarun Bozra."
13 Ga abin da UBANGIJI ya ce,
"Saboda zunubai uku na Ammon,
har guda huɗu ma, ba zan fasa hukunta shi ba.
Don ya tsaga cikin matan Gileyad masu juna biyu
don kawai yă ƙwace ƙasar.
14 Zan sa wuta a katangar Rabba
da za tă ƙone kagarunta
za a yi kururuwa a ranar yaƙi,
faɗan kuwa zai yi rugugi kamar hadiri.
15 Sarkinta§ zai je bauta,
shi da ma'aikatansa,"
in ji UBANGIJI.

# 2

1 Ga abin da UBANGIJI ya ce,
"Saboda zunubai uku na Mowab,
har guda huɗu ma, ba zan fasa hukunta su ba.
Gama ya ƙone ƙasusuwan sarkin Edom
suka zama sai ka ce toka.
2 Zan sa wuta a Mowab
da za tă ƙone kagarun Keriyot*
Mowab za tă gangara cikin hayaniya mai girma
cikin kururuwar yaƙi da kuma ƙarar ƙaho.
3 Zan hallaka mai mulkinta
zan kuma kashe shugabanninta."
4 Ga abin da UBANGIJI ya ce,
"Saboda zunubai uku na Yahuda,
har guda huɗu ma, ba zan fasa hukunta su ba.
Gama sun ƙi bin dokar UBANGIJI
ba su kuma yi biyayya da ƙa'idodinsa ba,
domin allolin ƙarya sun ruɗe su,
allolin da kakanninsu suka bauta.
5 Zan sa wuta a Yahuda
da za tă ƙone kagarun Urushalima."

### *Hukunci a kan Isra'ila*

6 Ga abin da UBANGIJI ya ce,
"Saboda zunubai uku na Isra'ila,
har guda huɗu ma, ba zan fasa hukunta su ba.
Don sun sayar da adalai waɗanda
suka kāsa biyan bashinsu.
Sun kuma sayar da matalauta
waɗanda bashinsu bai ma kai ko kuɗin bi-labi ba.
7 Sun tattake kawunan matalauta
kamar yadda suke taka laka
suka kuma danne wa marasa galihu gaskiya.

§ **1:15** Ko kuwa Molek; Ibraniyawa malkam * **2:2** Ko kuwa na biranenta

Uba da ɗa su na kwana da yarinya guda,
suna kuma ɓata sunana mai tsarki.
8 Suna kwanciya kurkusa da kowane bagade
a kan tufafin da suka karɓe jingina.
A gidajen allolinsu
sukan sha ruwan inabin da suka karɓo daga wurin waɗanda suka ci wa tara.

9 “Na hallaka mutumin Amoriyawa a gabansu,
ko da yake ya yi dogo kamar itacen al’ul
kuma mai ƙarfi kamar itacen oak.
Na hallaka ’ya’yan itatuwansa daga sama,
da kuma jijiyoyinsa daga ƙasa.
10 Na fitar da ku daga ƙasar Masar,
na kuma bishe ku tsawon shekaru arba’in a cikin hamada
don in ba ku ƙasar Amoriyawa.

11 “Na kuma tā da annabawa daga cikin ’ya’yanku maza
waɗansu kuma su zama keɓaɓɓu daga cikin samarinku.
Ba haka ba ne, mutanen Isra’ila?”
In ji Ubangiji.
12 “Amma kuka sa keɓaɓɓun suka sha ruwan inabi
kuka kuma umarci annabawa kada su yi annabci.

13 “Saboda haka, yanzu zan murƙushe ku
kamar yadda amalanke yakan murƙushe sa’ad da aka yi masa labtun hatsi.
14 Masu gudu da sauri ba za su tsira ba,
masu ƙarfi ba za su iya yin amfani da ƙarfinsu ba,
jarumi kuma ba zai iya ceton ransa ba.
15 ’Yan baka ba za su iya dāgewa ba,
masu saurin gudu ba za su tsira ba
mahayin dawakai kuma ba zai tsere da ransa ba.
16 Ko jarumawa mafi jaruntaka
za su gudu tsirara a ranan nan,”
in ji Ubangiji.

# 3

*An kira shaidu a kan Isra’ila*

1 Ku ji wannan maganar da Ubangiji ya yi game da ku, ya ku jama’ar Isra’ila, a kan
dukan iyalin da na fitar daga Masar.
2 “Ku ne kaɗai na zaɓa
cikin dukan al’umman duniya;
saboda haka zan hukunta ku
saboda dukan zunubanku.”

3 Mutum biyu za su iya yin tafiya tare
in ba su yarda su yi haka ba?
4 Zaki yakan yi ruri a jeji
in bai sami kama nama ba?
Zai yi gurnani a cikin kogonsa
in bai kama kome ba?
5 Tsuntsu yakan fāɗa a tarko a ƙasa
inda ba a sa tarko ba,

ko tarko yakan zargu daga ƙasa
in ba abin da ya taɓa shi?
6 Idan aka busa ƙaho a ciki birni
mutane ba sa yin rawar jiki?
Sa'ad da bala'i ya auko wa birni,
ba UBANGIJI ne ya sa a kawo shi ba?

7 Ba shakka, UBANGIJI Mai Iko Duka ba ya yin wani abu
ba tare da ya sanar wa bayinsa annabawa ba.

8 Zaki ya yi ruri,
wa ba zai tsorata ba?
UBANGIJI Mai Iko Duka ya yi magana,
wa ba zai yi annabci ba?

9 Ku yi shela ga kagarun Ashdod
da kuma ga kagarun Masar.
"Ku tara kanku a tuddan Samariya;
ku ga rashin jituwar da take a cikinta,
da kuma zaluncin da ake yi a cikin mutanenta."

10 "Ba su ma san yadda za su yi abin da yake daidai ba,"
in ji UBANGIJI,
"sun ɓoye ganima da abubuwan da suka washe a cikin kagarunsu."
11 Saboda haka ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka ya ce,
"Abokin gāba zai ƙwace ƙasar,
zai saukar da mafakarku,
zai washe kagarunku."
12 Ga abin da UBANGIJI ya ce,
"Kamar yadda makiyayi yakan ceci daga bakin zaki
ƙasusuwa ƙafafu biyu kawai ko kunne ɗaya,
haka za a ceci Isra'ilawa,
masu zama a Samariya
da kan gado kawai
da kuma a ɗan ƙyalle* a kan dogayen kujerunsu.†"
13 "Ku ji wannan ku kuma yi wa gidan Yaƙub gargaɗi," in ji UBANGIJI, UBANGIJI
Allah Maɗaukaki.
14 "A ranar da zan hukunta Isra'ila saboda zunubanta,
zan hallaka bagadan Betel;
za a yayyanka ƙahonin bagadan
za su fāɗa ƙasa
15 Zan rushe gidan rani
da na damina;
gidajen da aka yi musu ado da hauren giwa za a rushe su
haka ma duk za a rurrushe manyan gidaje,"
in ji UBANGIJI.

# 4

## *Isra'ila ba ta koma ga Allah ba*

* **3:12** Ma'anar kalmar Ibraniyancin nan babu tabbas. † **3:12** Ko kuwa Za a ceci Isra'ilawa / waɗanda suke zama a Samariya / a gefen gadajensu / da kuma a Damaskus kan kujerunsu

1 Ku kasa kunne ga wannan, ya ku shanun Bashan a kan Dutsen Samariya,
ku matan da kuke cin zalin matalauta, kuke kuma danne matalauta,
kuna kuma ce wa mazanku, “Ku kawo mana abin sha!”
2 UBANGIJI Mai Iko Duka ya rantse da tsarkinsa.
“Tabbatacce lokaci yana zuwa
da za a jawo ku da ƙugiyoyi,
na ƙarshenku za a kama da ƙugiyar kifi.
3 Dukanku za ku wuce ta kai tsaye
ta inda katangar ta tsage,
za a jefar da ku a Harmon,”*
in ji UBANGIJI.
4 “Ku tafi Betel ku yi ta aikata zunubi;
ku je Gilgal ku ƙara yin zunubi.
Ku kawo hadayunku kowace safiya,
zakkarku kowace shekara uku.†
5 Ku ƙona burodinku mai yisti kamar hadaya ta godiya,
ku yi fariya game da hadayunku na yarda rai,
ku yi taƙama game da su, ya ku Isra’ilawa,
gama abin da kuke jin daɗin aikata ke nan,”
in ji UBANGIJI Mai Iko Duka.

6 “Na bar ku da yunwa‡ a kowace birni,
da kuma rashin abinci a kowane gari,
duk da haka ba ku juyo gare ni ba,”
in ji UBANGIJI.

7 “Na kuma hana muku ruwan sama
tun shuke-shuken suna wata uku kafin lokacin girbi.
Na sa aka yi ruwan sama a wani gari,
sai na hana a yi a wani gari.
Wata gona ta sami ruwan sama;
wata gona kuma ta bushe.
8 Mutane suna tangaɗi daga gari zuwa gari suna neman ruwa
amma ba su sami isashen ruwan sha ba,
duk da haka ba ku juyo gare ni ba,”
in ji UBANGIJI.

9 “Sau da yawa na ɓata gonakinku
da fumfuna da kuma cuta.
Fāri suka cinye itatuwanku na inabi da na ɓaure, da na zaitun
duk da haka ba ku juyo gare ni ba,”
in ji UBANGIJI.

10 “Na aiko muku annoba
yadda na yi a Masar.
Na karkashe samarinku da takobi,
tare da kamammun dawakanku.
Na cika hancinku da warin sansaninku,
duk da haka ba ku juyo gare ni ba”

* **4:3** Rubuce-rubucen hannu na Masoretik; da ɓangare dabam na kalmar Ibraniyanci (dubi Seftuwajin) waje, ya dutsen danniya † **4:4** Ko kuwa zakka a rana ta uku ‡ **4:6** Ibraniyanci ku da tsabtar haƙora

in ji UBANGIJI.

11 “Na hallaka waɗansunku
kamar§ yadda na hallaka Sodom da Gomorra.
Kuna kama da itace mai cin wutar da na cire daga cikin wuta,
duk da haka ba ku juyo gare ni ba,”
in ji UBANGIJI.

12 “Saboda haka ga abin da zan yi da ku, ya Isra’ila,
don kuwa zan yi muku haka,
sai ku yi shirin gamuwa da Allahnku, ya Isra’ila.”

13 Shi wanda ya yi duwatsu,
ya halicci iska,
ya kuma bayyana wa mutum tunaninsa,
shi wanda ya juya safiya ta zama duhu
yana takawa a wurare masu tsawo na duniya,
UBANGIJI Allah Maɗaukaki ne sunansa.

# 5

*Makoki da kuma kira ga tuba*

1 Ku ji wannan magana, ya gidan Isra’ila, ina makokin nan dominku.
2 “Budurwa Isra’ila ta fāɗi,
ba za tă ƙara tashi ba,
an yashe ta a ƙasarta,
ba wanda zai ɗaga ta.”
3 Ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka ya ce,
“Birnin da ta fitar da masu ƙarfi dubbai don Isra’ila
guda ɗari kaɗai za su dawo;
garin da ya fitar da masu ƙarfi ɗari kuwa
goma kaɗai za su dawo.”
4 Ga abin da UBANGIJI ya ce wa gidan Isra’ila.
“Ku neme ni ku rayu;
5 kada ku nemi Betel,
kada ku je Gilgal,
kada ku yi tafiya zuwa Beyersheba.
Gama ba shakka Gilgal za tă tafi bauta,
za a kuwa mai da Betel ba kome ba.”*
6 Ku nemi UBANGIJI ku kuma rayu,
ko kuwa zai ratsa yă share gidan Yusuf kamar wuta;
zai cinye
Betel kuwa ba zai sami wanda zai kashe ta ba.

7 Ku ne masu mai da gaskiya ta koma ɗaci
ku kuma zubar da adalci.

8 (Shi wanda ya yi Taurarin nan da ake ce Kaza da ’Ya’yanta da kuma Mai Farauta da Kare,
wanda ya mai da duhu ya zama haske

§ **4:11** Ibraniyanci Allah * **5:5** Ko kuwa baƙin cikin; Ko kuwa mugunta; Da Ibraniyanci awen, kwatanci ga Bet Awen (wani sunan reni don Betel).

ya kuma baƙanta rana ta zama dare,
yakan kwashe ruwan teku
ya zubar a ƙasa,
Ubangiji ne sunansa,
9 yakan kawo hallaka a mafaka mai ƙarfi
yakan kuma mai da birnin mai katanga ya zama kufai).

10 Ba ku son mai yin gaskiya a ɗakin shari'a
kuna ƙin mai faɗar gaskiya.

11 Kuna matsa wa matalauta
kuna sa su dole su ba ku hatsi.
Saboda haka, ko da yake kun gina gidajen duwatsu,
ba za ku zauna a cikinsu ba;
ko da yake kun nome gonaki masu kyau,
ba za ku sha ruwan inabinsu ba.
12 Gama na san yawan laifofinku
da kuma girman zunubanku.

Kuna danne masu adalci kuna kuma cin hanci
kuna kuma hana a yi wa matalauta shari'ar adalci a majalisa.
13 Saboda haka mai hankali yakan yi shiru a lokuta kamar haka,
gama lokutan mugaye ne.

14 Ku yi nagarta, ba mugunta ba;
don ku rayu
sa'an nan Ubangiji Allah Maɗaukaki zai kasance da ku,
kamar yadda kuka ce zai yi.
15 Ku ƙi mugunta, ku ƙaunaci nagarta;
ku dinga yin shari'ar gaskiya a ɗakunan shari'a.
Mai yiwuwa Ubangiji Allah Maɗaukaki zai ji tausayin
raguwar Yusuf.
16 Saboda haka ga abin da Ubangiji, Ubangiji Allah Maɗaukaki yana cewa,
"Za a yi kururuwa a dukan tituna
a kuma yi kuka don azaba a dukan wuraren da jama'a sukan taru.
Za a yi kira ga manoma su yi kuka
masu makoki kuma su yi kuka.
17 Za a yi kuka a dukan gonakin inabi,
gama zan ratsa a cikinku,"
in ji Ubangiji.

### *Ranar Ubangiji*

18 Kaitonku masu son
ganin ranar Ubangiji!
Don me kuke son ganin ranar Ubangiji?
Za a duhunta ranan nan, ba haske ba.
19 Za ku zama kamar mutanen da suka guje wa zaki
sai suka fāɗa a hannun beyar,
ko kuma kamar wanda ya shiga gida
ya dāfa hannu a bango
sai maciji ya sare shi.
20 Ashe, ranar Ubangiji ba duhu ba ce, a maimakon haske,

duhu wuluk, ba tare da ko ɗan haske ba.

21 “Na ƙi, ina kuma ƙyamar bukukkuwanku na addini;
ba na son ganin tarurrukanku.
22 Ko da kun kawo mini hadayu na ƙonawa da kuma hadayu na hatsi,
ba zan karɓa ba.
Ko da kun kawo zaɓaɓɓun hadayu na zumunta,
ba zan ɗauke su a bakin kome ba.
23 Ku tashi daga nan da surutan waƙoƙinku!
Ba zan saurari kaɗe-kaɗe da bushe bushenku ba.
24 Amma bari gaskiya ta kwararo kamar kogi,
adalci kuma kamar rafin da ba ya taɓa bushewa!

25 “Kun kawo mini hadayu da sadakoki
shekaru arba’in a cikin jeji, ya ku gidan Isra’ila?
26 Kun ɗaga masujadar sarkinku,
siffofin gumakanku,
tauraron allahnku,†
wanda kuka yi wa kanku.
27 Saboda haka zan tura ku zaman bauta gaba da Damaskus,”
in ji Ubangiji, wanda sunansa ne Allah Mai Iko.

# 6

## *Kaito ga zaman sakewa*

1 Taku ta ƙare, ku da kuke zaman sakewa a Sihiyona,
da ku waɗanda kuke ji zama a Dutsen Samariya lafiya ne,
ku manyan mutanen ƙasar da take sananniya,
waɗanda mutanen Isra’ila suke zuwa!
2 Ku je Kalne ku dube ta;
ku wuce daga can zuwa Hamat-rabba,
sa’an nan ku gangara zuwa Gat a Filistiya.
Sun fi masarautunku biyu ne?
Kasarsu ta fi taku girma?
3 Kuna ƙoƙari ku kauce wa wannan muguwar rana
kuna kuma jawo mulkin tashin hankali kusa.
4 Kuna kwanciya a kan gadajen da aka yi musu shimfiɗar hauren giwa
kuna mimmiƙe a kan kujerunku.
Kuna cin naman ƙibabbun raguna
da na ƙosassun ’yan maruƙa.
5 Kuna kaɗa molayenku yadda Dawuda ya yi
kuna ƙirƙiro waƙoƙi a kan kayan kaɗe-kaɗe.
6 Da manyan kwanoni kuke shan ruwan inabi
kuna kuma shafa mai mafi kyau,
amma ba kwa baƙin ciki game da kangon da Yusuf ya zama.
7 Saboda haka za ku zama na farkon da za su tafi zaman bauta;
bukukkuwanku da shagulgulanku za su ƙare.

## *Ubangiji yana ƙyamar girmankan Isra’ila*

8 Ubangiji Mai Iko Duka da kansa ya rantse, Ubangiji Allah Maɗaukaki ya furta,

† **5:26** Ko kuwa ɗaga Sakkut sarkinku da Kaiwan gumakanku, tauraron da suke allolinku; Seftuwajin ɗaga masujadar Molek da tauraro allahnku Refan, gumakansu

"Ina ƙyamar girman kan Yaƙub,
ba na kuma son kagarunsa;
zan ba da birnin
da duk abin da yake cikinta."
9 Ko da mutum goma ne suka ragu a gida guda, su ma za su mutu. 10 In kuma wani
dangi ya shiga don yă fitar da gawawwakin yă ƙone ya kuwa tambayi wani wanda
yake ɓoye a can, yana cewa, "Akwai wani tare da kai?" Ya kuwa ce, "Babu," sai yă
ce, "Kul! Kada mu ambaci sunan UBANGIJI."
11 Gama UBANGIJI ya ba da umarni,
zai kuma ragargaza babban gidan nan kucu-kucu
ƙaramin gidan kuwa zai yi rugu-rugu da shi.

12 Dawakai sukan yi gudu a kan duwatsu?
Wani yana iya yin noma a teku da shanun noma?
Amma ga shi kun mai da gaskiya ta zama dafi
amfanin adalci kuma ya zama ɗaci,
13 ku da kuke murna saboda an ci Lo Debar* da yaƙi
kuka kuma ce, "Ba da ƙarfinmu ne muka ƙwace Karnayim† ba?"

14 Gama UBANGIJI Allah Maɗaukaki ya ce,
"Zan sa wata ƙasa ta tayar muku, ya ku gidan Isra'ila,
wadda za tă matsa muku tun
daga Lebo‡ Hamat zuwa kwarin Araba."

# 7

*Fāri, wuta, da igiyar gwaji*

1 Ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka ya nuna mini. UBANGIJI yana shirya cincirindon
fāri bayan da aka ƙarasa yankan rabon hatsin da yake na sarki, hatsi na biyu kuma
yake tohuwa. 2 Sa'ad da suka cinye kome, sai na yi kira, na ce, "UBANGIJI Mai Iko
Duka, ka gafarta! Ta yaya Yaƙub zai tsira? Ga shi ɗan ƙarami ne!"
3 Saboda haka sai UBANGIJI ya dakatar da nufinsa.
"Wannan ba zai faru ba," in ji UBANGIJI.
4 Ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka ya nuna mini. UBANGIJI Mai Iko Duka yana
shirin hukunta da wuta; wutar ta ƙone teku ta kuma ƙone ƙasa. 5 Sai na yi kira, na
ce, "UBANGIJI Mai Iko Duka, ina roƙonka ka dakata! Ta yaya Yaƙub zai tsira? Ga shi
ɗan ƙarami ne!"
6 Saboda haka sai UBANGIJI ya dakatar da nufinsa.
"Wannan ma ba zai faru ba," in ji UBANGIJI Mai Iko Duka.

7 Ga abin da ya nuna mini. Ubangiji yana tsaye kusa da bangon da aka gina, bisa
ga awon igiyar gwada gini, da kuma magwaji a hannunsa. 8 Sai UBANGIJI ya tambaye
ni, "Me kake gani, Amos?"
Sai na amsa, "Igiyar gwada gini."
Sa'an nan Ubangiji ya ce, "Duba, zan sa igiyan nan a cikin mutanena Isra'ila; ba
zan ƙara barinsu ba.
9 "Za a hallakar da wuraren sujada na Ishaku
kuma tsarkakan wurare na Isra'ila za su zama kango;
da takobina zan tayar wa gidan Yerobowam."

* **6:13** Lo Debar yana nufin wofi. † **6:13** Karnayim yana nufin ƙahoni; ƙaho a nan yana a matsayin ƙarfi.
‡ **6:14** Ko kuwa daga mashigi zuwa

### *Amos da Amaziya*

10 Sai Amaziya firist na Betel ya aika da saƙo zuwa wurin Yerobowam sarkin Isra'ila.
"Amos yana shirya maka maƙarƙashiya a tsakiyar Isra'ila. Kasar ba za tă iya ɗauka
abubuwan da yake faɗi ba. 11 Gama ga abin da Amos yake cewa,
" 'Yerobowam zai mutu ta wurin takobi,
kuma tabbatacce Isra'ila za su tafi zaman bauta,
nesa da ainihin ƙasarsu.' "
12 Sai Amaziya ya ce wa Amos, "Tafi daga nan, mai duba kawai! Koma ƙasar
Yahuda. Ka nemi abin zaman garinka a can ka kuma yi annabcinka a can. 13 Kada
ka ƙara yin annabci a Betel, gama nan wuri mai tsarki ne na sarki da kuma haikalin
ƙasar."
14 Amos ya amsa wa Amaziya, "Ni ba annabi ba ne ko ɗan annabi, amma ni
makiyayi ne, kuma ina lura da itatuwan al'ul. 15 Amma UBANGIJI ya ɗauke ni daga
kiwon dabbobi ya ce mini, 'Je ka, ka yi wa mutanena Isra'ila annabci.' 16 Yanzu fa,
sai ka ji maganar UBANGIJI. Ka ce,
" 'Kada in yi annabci a kan Isra'ila,
kuma in daina yin wa'azi a kan gidan Ishaku.'
17 "Saboda haka ga abin da UBANGIJI ya ce,
" 'Matarka za tă zama karuwa a cikin birni,
kuma da takobi za a kashe 'ya'yanka maza da mata.
Za a auna ƙasarka a kuma raba ta,
kai kuma za ka mutu a ƙasar arna.*
Ba shakka Isra'ila za su tafi zaman bauta,
nesa da ainihin ƙasarsu.' "

## 8

### *Kwandon nunannun 'ya'yan itace*

1 Ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka ya nuna mini. UBANGIJI ya nuna mini kwandon
nunannun 'ya'yan itace. 2 Ya yi tambaya ya ce, "Me ka gani Amos?"
Sai na amsa na ce, "Kwandon nunannun 'ya'yan itace."
Sai UBANGIJI ya ce mini, "Lokaci ya yi wa mutanena Isra'ila da ba zan ƙara barinsu
ba.
3 "A ranan nan," in ji UBANGIJI Mai Iko Duka, "Waƙoƙin a haikali za su koma
makoki.* Za a ga gawawwaki a ko'ina! Shiru!"
4 Ku ji wannan, ku da kuke tattake masu bukata
kuka kori matalautan ƙasar.
5 Kuna cewa,
"Yaushe Sabon Wata zai wuce
don mu sayar da hatsi,
Asabbaci ta wuce,
don mu sayar da alkama?"
Mu yi awo da ma'aunin zalunci
mu ƙara kuɗin kaya
mu kuma cutar da mai saya,
6 mu sayi matalauta da azurfa
masu bukata kuma da takalmi,
mu sayar da alkamar haɗe da yayi.
7 UBANGIJI ya rantse da Girman Yaƙub, "Ba zan taɓa mantawa da duk wani abin da
suka yi ba.
8 "Shin, ƙasar ba za tă yi rawan jiki saboda wannan ba,

* **7:17** Da Ibraniyanci marasa tsabta * **8:3** Ko kuwa "mawaƙar haikali za su yi makoki"

kuma duk masu zama a cikinta ba za su yi makoki ba?
Kasar duka za tă hau ta sauka kamar Nilu;
za a dama ta sa'an nan ta nutse
kamar kogin Masar.
9 "A wannan rana," in ji UBANGIJI Mai Iko Duka,
"Zan sa rana ta fāɗi da tsakar rana
in kuma duhunta duniya da rana tsaka.
10 Zan mai da bukukkuwanku na addini su zama makoki
kuma dukan waƙoƙinku su zama kuka.
Zan sa dukanku ku sa rigunan makoki
za ku kuma aske kawunanku.
Zan sa wannan lokaci yă zama kamar lokacin da ake makokin ɗan tilon da ake da shi
kuma ƙarshenta kamar rana mai ɗaci.

11 "Ranakun suna zuwa," in ji UBANGIJI Mai Iko Duka,
"sa'ad da zan aika da yunwa cikin ƙasar,
ba yunwar abinci ko ta ƙishirwa ba,
sai dai yunwa ta jin maganar UBANGIJI.
12 Mutane za su yi ta tangaɗi daga teku zuwa teku
suna yawo daga arewa zuwa kudu,
suna neman maganar UBANGIJI,
amma ba za su samu ba.
13 "A wannan rana
"kyawawan 'yan mata da kuma samari masu ji da ƙarfi
za su suma don ƙishirwa.
14 Waɗanda suka yi rantsuwa da abin kunya† na Samariya,
ko kuma su ce, 'Muddin allahnku yana a raye, ya Dan,'
ko kuwa, 'Muddin allahn‡ Beyersheba yana a raye,'
za su fāɗi,
ba kuwa za su ƙara tashi ba."

# 9

*Za a hallaka Isra'ila*

1 Na ga Ubangiji yana tsaye a gaban bagade, ya kuma ce,
"Bugi kan ginshiƙan
don madogaran ƙofa su girgiza.
Saukar da su a kan dukan mutane;
waɗanda ba su mutu ba zan kashe su da takobi.
Ba mutum guda da zai tsere,
babu wani da zai tsira.
2 Ko da sun tona rami kamar zurfin kabari,
daga can hannuna zai fitar da su.
Ko da sun hau can sama
daga can zan sauko da su.
3 Ko da sun ɓuya a bisa Karmel,
a can zan farauce su in cafko.
Ko da sun ɓuya can ƙarƙashin teku,
a can zan umarci maciji yă sare su.
4 Ko da abokan gābansu sun kore su zuwa zaman bauta,
a can zan umarci takobi yă kashe su.

† **8:14** Ko kuwa da Ashima; ko da gunki ‡ **8:14** Ko kuwa iko

“Zan sa musu ido
don mugunta ba don alheri ba.”

5 Ubangiji, UBANGIJI Maɗaukaki,
shi da yakan taɓa ƙasa sai ta narke,
kuma dukan mazauna cikinta suna makoki,
ƙasar gaba ɗaya takan hau ta kuma sauka kamar Nilu,
sa’an nan ta nutse kamar kogin Masar,
6 shi da ya gina kyakkyawar fadarsa* a cikin sammai
ya kuma kafa harsashenta† a duniya,
shi da yakan kira ruwan teku
yă kuma kwarara su a bisa duniya,
UBANGIJI ne sunansa.

7 “Ku ba Isra’ilawa ba ne,
daidai gare ni kamar yadda Kushawa suke?”‡
In ji UBANGIJI.
“Ban fito da Isra’ila daga Masar ba,
Filistiyawa kuma daga Kaftor§
Arameyawa kuma daga Kir ba?

8 “Tabbatacce idanun UBANGIJI Mai Iko Duka
suna a kan mulkin nan mai zunubi.
Zan hallaka shi
daga fuskar duniya,
duk da haka ba zan hallaka
gidan Yaƙub ƙaƙaf ba,”
in ji UBANGIJI.
9 “Gama zan ba da umarni,
zan kuma tankaɗe gidan Isra’ila
a cikin dukan ƙasashe
kamar yadda ake tankaɗe hatsi a cikin matankaɗi
kuma ko ƙwaya ɗaya ba za tă fāɗi a ƙasa ba.
10 Dukan masu zunubi a cikin mutanena
za su mutu ta wurin takobi,
wato, su masu cewa,
‘Masifa ba za tă fāɗo ko ta same mu ba.’

### *Maidowar Isra’ila*

11 “A wannan rana zan maido
da tentin Dawuda da ya fāɗi.
Zan gyaggyara wuraren da suka yayyage,
in kuma maido da kufansa
in gina shi kamar yadda yake a dā,
12 domin su mallaki raguwar Edom
da duk al’ummai da suke amsa sunana,”*
in ji UBANGIJI shi wanda zai yi waɗannan abubuwa.
13 “Ranaku suna zuwa, in ji UBANGIJI,
“sa’ad da mai huɗa zai sha gaban mai girbi

* **9:6** Ma’anar Ibraniyanci don wannan zance babu tabbas. † **9:6** Ma’anar Ibraniyanci don wannan kalma babu tabbas. ‡ **9:7** Wato, mutane daga yankin bisa na Nilu § **9:7** Wato, Kirit * **9:12** Da Ibraniyanci; Seftuwajin don raguwar mutane / da kuma dukan al’umman da ake kira da sunana za su nemi Ubangiji

mai shuki kuma yă bi bayan mai matsin inabi.
Sabon ruwan inabi zai ɗiga daga duwatsu
yă kuma kwararo daga tuddai.
14 Zan dawo da waɗanda aka kai zaman bauta† mutanena Isra'ila.

"Za su sāke gina biranen da suke kango su kuma zauna a cikinsu.
Za su shuka gonakin inabi su kuma sha ruwan inabinsu;
za su yi lambuna su kuma ci amfaninsu.
15 Zan dasa Isra'ila a ƙasarsu,
ba kuwa za a ƙara tumɓuke su
daga ƙasar da na ba su ba,"
in ji UBANGIJI Allahnku.

† **9:14** Ko kuwa zan maido da nasarar

# Obadiya

1 Wahayin Obadiya.

Ga abin da UBANGIJI Mai Iko Duka ya ce a kan Edom.
Mun ji saƙo daga wurin UBANGIJI cewa,
An aiki jakada zuwa ga al'ummai yă faɗa musu cewa,
"Ku tashi, mu tafi mu yi yaƙi da ita."

2 "Duba, zan maishe ki ƙarama a cikin al'ummai;
za a rena ki ƙwarai.
3 Fariyar zuciyarki ta yaudare ki,
ke da kike zama can bisa duwatsu*
kika kuma yi gidanki a kan ƙwanƙoli,
ke da kike ce wa kanki,
'Wa zai iya saukar da ni ƙasa?'
4 Ko da yake kina firiya kamar gaggafa
kin kuma yi sheƙarki a can cikin taurari,
daga can zan saukar da ke,"
in ji UBANGIJI.
5 "In ɓarayi suka zo miki,
in kuma 'yan fashi suka shigo gidan da dare,
kash, bala'i zai jira ki
ba abin da suke so ne kawai za su sata ba?
In kuma masu tsinka 'ya'yan inabi suka zo miki,
ba sukan bar 'ya'yan inabi kaɗan ba?
6 Amma za a washe Isuwa ƙaƙaf,
a kuma yaye ɓoyayyiyar dukiyarsa!
7 Dukan waɗanda kike tarayya da su, za su kore ki zuwa iyaka;
abokanki kuma za su yaudare ki, su kuma sha ƙarfinki;
waɗanda suke cin abincinki, za su sa miki tarko,†
amma ba za ki gane ba.

8 "A wannan rana," in jin UBANGIJI,
"zan hallaka masu hikimar Edom,
zan shafe mutane masu fahima a duwatsun Isuwa.
9 Jarumawanki, ya Teman, za su razana,
za a kashe kowane mutum a duwatsun Isuwa.
10 Saboda halin kama-karyar da kika yi wa ɗan'uwanka Yaƙub,
za ki sha kunya;
za a hallaka ki har abada.
11 A ranan nan kin tsaya kawai kina zuba ido
yayinda baƙi suke washe dukiyar ɗan'uwanki,
baƙi kuma suka shiga ta ƙofofinsa
suka jefa ƙuri'a don a rarraba Urushalima,
kin tsaya kina kallo kamar ɗaya daga cikin abokan gābansa.
12 Bai kamata ki rena ɗan'uwanki

* 1:3 Ko kuwa na Sela † 1:7 Ma'anar Ibraniyanci don wannan babu tabbas.

a ranar masifarsa ba,
ko ki yi farin ciki a kan mutanen Yahuda
a ranar hallakarsu,
ko ki yi fariya sosai
a ranar wahalarsu.
13 Bai kamata ki bi ta ƙofofin mutanena
a ranar bala'insu ba,
ko ki rena su a cikin masifarsu
a ranar bala'insu,
ko ki ƙwace dukiyarsu
a ranar bala'insu ba.
14 Bai kamata ki tsaya a mararraba
don ki kashe waɗanda suke ƙoƙarin tserewa ba,
ko ki ba da waɗanda suka tsere ga hannun maƙiyansu
a ranar wahalarsu ba.

15 "Ranar UBANGIJI ta yi kusa
don dukan al'ummai.
Kamar yadda kuka yi, haka za a yi muku;
ayyukanku za su koma a kanku.
16 Kamar yadda kuka sha a kan tuduna mai tsarki,
haka dukan al'ummai za su yi ta sha,
za su sha, su kuma sha
su zama sai ka ce ba su taɓa kasancewa ba.
17 Amma a kan Dutsen Sihiyona za a sami ceto;
Dutsen zai zama mai tsarki,
gidan Yaƙub kuma
zai mallaki gādonsa.
18 Gidan Yaƙub zai zama kamar wuta,
gidan Yusuf kuma kamar harshen wuta;
gidan Isuwa zai zama kamar tattaka,
za a kuma sa masa wuta yă ƙone.
Babu wanda zai tsira
daga gidan Isuwa."
Ni UBANGIJI na faɗa.

19 Mutane daga Negeb za su mamaye
duwatsun Isuwa,
mutane kuma daga gindin tuddai za su mallaki
ƙasar Filistiyawa.
Za su mamaye filayen Efraim da Samariya,
Benyamin kuwa zai mallaki Gileyad.
20 Wannan ƙungiyar Isra'ilawan da aka kwashe zuwa bauta da suke a Kan'ana
za su mallaki ƙasar har zuwa Zarefat;
waɗannan da aka kwashe zuwa bauta daga Urushalima da suke a Sefarad
za su mallaki garuruwan Negeb.
21 Masu kawo ceto za su haura zuwa‡ Dutsen Sihiyona
don su yi mulkin duwatsun Isuwa.
UBANGIJI ne zai yi mulki.

‡ **1:21** Ko kuwa daga

# Yunana

*Yunana ya gudu daga Ubangiji*

1 Maganar Ubangiji ta zo wa Yunana ɗan Amittai cewa, 2 “Tafi babban birnin nan
Ninebe ka yi mata wa’azi, saboda muguntarta ta haura zuwa gabana.”
3 Amma Yunana ya gudu daga Ubangiji ya nufi Tarshish. Ya gangara zuwa Yaffa,
inda ya sami jirgin ruwa mai shirin tashi daga tashar. Bayan ya biya kuɗin tafiya,
sai ya shiga jirgi ya kama hanya zuwa Tarshish don yă tsere wa Ubangiji.
4 Sai Ubangiji ya aika da babban iska a bisan teku, hadiri ya tsananta ƙwarai har
jirgin ya yi barazanar farfashewa. 5 Dukan matuƙan jirgin suka tsorata, kowannensu
kuma ya yi kuka ga allahnsa, suka kuma jefar da kayan jirgi a cikin teku domin su
rage nauyin jirgin.
Ana cikin haka, ashe, Yunana ya sauka can ƙarƙashin jirgi ya je ya kwanta, yana
ta sharar barcinsa. 6 Sai kyaftin ɗin ya je wajensa ya ce masa, “Don me kake barci?
Tashi ka kira bisa ga allahnka! Mai yiwuwa yă ji mu, yă cece mu don kada mu
hallaka.”
7 Matuƙan jirgin suka ce wa juna, “Ku zo, mu jefa ƙuri’a mu ga wa ke da alhakin
wannan masifa.” Sai suka jefa ƙuri’a, ƙuri’ar kuwa ta fāɗa a kan Yunana. 8 Saboda
haka suka tambaye shi suka ce, “Yanzu, gaya mana, dalilin da ya sa wannan masifa
ta zo mana? Mene ne aikinka? Daga ina ka fito? Ina ne ƙasarka? Daga wacce kabila
ce ka fito?”
9 Sai ya amsa, “Ni mutumin Ibraniyawa ne, ina kuma bauta wa Ubangiji Allah na
sama, wanda ya yi teku da tuddai.”
10 Sai matuƙan jirgin suka tsorata ƙwarai, suka ce masa, “Wane irin mugun abu ne
ka aikata haka?” (Sun gane cewa yana gudu ne daga wurin Ubangiji, domin ya riga
ya faɗa musu.)
11 Sai tekun ya daɗa rikicewa. Sai suka tambaye shi, “Me za mu yi da kai domin
tekun yă daina hauka?”
12 Ya amsa musu ya ce, “Ku ɗauke ni ku jefa a cikin teku, tekun zai kwanta. Na san
cewa laifina ne ya jawo wannan babban hadirin da ya auka muku.”
13 Maimakon mutanen su yi haka, sai suka yi ƙoƙari su tura jirgin ruwan zuwa
bakin teku. Amma ba su iya ba, saboda iskar ta sa tekun ya yi ta ƙara hauka. 14 Sai
suka yi kuka ga Ubangiji suka ce, “Ya Ubangiji, in ka yarda kada ka bar mu mu mutu
saboda ran mutumin nan. Kada ka yi mana hukuncin masu kisankai, gama kai ne,
ya Ubangiji, ka ga ya gamshe ka.” 15 Sa’an nan suka ɗauki Yunana suka jefar da
shi daga jirgin, sai tekun ya kwanta. 16 Ganin haka sai mutanen suka cika da tsoron
Ubangiji, suka kuma miƙa wa Ubangiji hadaya, suka yi wa’adi da shi.

*Addu’ar Yunana*

17 Amma Ubangiji ya tanada wani babban kifi da zai haɗiye Yunana, Yunana kuwa
ya yi yini uku da dare uku a ciki cikin kifin.

## 2

1 Daga ciki cikin kifi, Yunana ya yi addu’a ga Ubangiji Allahnsa. 2 Ya ce,

“A cikin damuwata na yi kira ga Ubangiji,
ya kuwa amsa mini.
Daga cikin zurfi kabari* na yi kiran neman taimako,
ka kuwa saurari kukata.

---

* **2:2** Sheol na Ibraniyanci

3 Cikin tashin hankali, ka jefa ni cikin zurfafa, a tsakiyar teku,
ka kuma jujjuya ni a cikin ruwa;
dukan raƙuman ruwanka da ambaliyarka
sun bi ta kaina.
4 Sai na ce, 'An kore ni
daga fuskarka;
duk da haka zan sāke duba
wajen haikalinka mai tsarki.'
5 Ruwayen da suke kewaye da ni sun yi mini barazana,†
zurfi kuma ya kewaye ni, ciyayin ruwa suna nannaɗe kewaye da ni.
6 Na nutsa har ƙarƙashin tuddai;
a ƙarƙashin duniya, ka rufe ni har abada.
Amma ka dawo da raina daga rami,
Ya Ubangiji Allahna.

7 "Sa'ad da na ji raina yana rabuwa da ni,
na tuna da kai ya Ubangiji,
addu'ata kuma ta kai gare ka,
a haikalinka mai tsarki.

8 "Waɗanda suka maƙale wa gumaka marasa amfani,
sukan ƙyale alherin da zai kasance nasu.
9 Amma ni, da waƙar godiya,
zan miƙa tawa hadaya gare ka.
Abin da na yi alkawari, shi ne zan yi.
Ceto yakan zo ne kawai daga wurin Ubangiji."
10 Sai Ubangiji ya umarci kifin, kifin kuwa ya amayar da Yunana a gaɓan teku.

# 3

*Yunana ya tafi Ninebe*

1 Sa'an nan sai maganar Ubangiji ta zo wa Yunana sau na biyu. 2 "Tafi babban
birnin nan Ninebe, ka yi masa shelar saƙon da na ba ka."
3 Sai Yunana ya yi biyayya da maganar Ubangiji, ya tafi Ninebe. Ninebe birni ne
da yake da muhimmanci, wanda sai an ɗauki kwana uku kafin a iya zaga shi. 4 A
rana ta fari, Yunana ya kama tafiya yana ratsa birnin. Sai ya yi shela cewa, "Nan
da kwana arba'in za a hallaka Ninebe?" 5 Mutanen Ninebe kuwa suka gaskata Allah.
Aka yi shela a yi azumi, sai dukansu daga babba har zuwa ƙaraminsu, suka sa tufafin
makoki.
6 Da saƙon Yunana ya kai kunnen sarkin Ninebe, sai ya tashi daga kujerar mulkinsa,
ya tuɓe alkyabbarsa, ya sa rigar makoki, ya zauna cikin toka. 7 Sai ya yi umarni a
Ninebe cewa,
"Bisa ga umarnin sarki da fadawansa.
"Kada a bar wani mutum ko dabba, garke ko shannu, su ɗanɗana wani abu; kada
a bari su ci ko su sha. 8 Bari kowane mutum da dabba yă yafa rigunan makoki.
Kowa yă roƙi Allah da gaske, kowa kuma yă bar mugayen ayyukan da yake yi. 9 Wa
ya sani? Ko Allah zai ji tausayinmu da kuma juyayinmu yă janye zafin fushinsa
don kada mu hallaka."
10 Da Allah ya ga abin da suka yi, da kuma yadda suka juya daga mugayen
hanyoyinsu sai ya ji tausayinsu, bai kawo hallaka a kansu yadda ya yi shirin yi ba.

† **2:5** Ko kuwa ruwaye sun kai ga maƙoshina

# 4

### *Fushin Yunana a kan tausayin Allah*

1 Sai abin ya ɓata wa Yunana rai ƙwarai har ya yi fushi. 2 Sai ya yi addu'a ga
UBANGIJI ya ce, “Ya UBANGIJI, ba irin abin da na faɗa ke nan ba tun ina gida? Wannan
ne ya sa na yi ƙoƙarin tserewa zuwa Tarshish. Ai, na sani kai Allah ne mai alheri da
tausayi, mai jinkirin fushi da cikakkiyar ƙauna, kai Allah ne mai dakatar da nufinka
na yin hukunci. 3 Yanzu, ya UBANGIJI, ka ɗauki raina, domin ya fi sauƙi a gare ni in
mutu da in rayu.”
4 Amma UBANGIJI ya amsa, ya ce; “Daidai ne ka yi fushi?”
5 Sai Yunana ya fita daga birnin ya yi wajen gabas, ya zauna. A nan ya yi wa
kansa rumfa, ya zauna cikin inuwarta yana jira yǎ ga abin da zai sami birnin. 6 Sai
UBANGIJI Allah ya sa wata 'yar kuringa ta tsiro, ta yi girma a inda Yunana yake, don ta
inuwantar da shi, yǎ ji daɗi. Yunana kuwa ya yi murna matuƙa da wannan kuringa.
7 Amma kashegari da safe sai Allah ya sa tsutsa ta cinye 'yar kuringar har ta mutu.
8 Sa'ad da rana ta yi sama, sai Allah ya sa iskar gabas mai zafi ta huro, zafin ranar
kuma ya buga kan Yunana, har ya ji sai ka ce zai suma. Ya so a ce ya mutu ma, sai
ya ce, “Gara in mutu da a ce ina zaune da rai.”
9 Amma Allah ya ce wa Yunana, “Daidai ne ka yi fushi saboda wannan kuringa?”
Sai Yunana ya ce, “I, daidai ne, ina fushi matuƙa, har ina so da na mutu ma.”
10 Sai UBANGIJI ya ce, “Ai, wannan kuringa ta tsira dare ɗaya ta kuma ɓace kafin
dare na biyu, ba ka yi wata wahala dominta ba, ba kai ne ka sa ta yi girma ba, duk
da haka ranka ya ɓace saboda ita. 11 Ashe, ba dole ne in ji tausayin babban birnin
nan Ninebe mai mutum sama da dubu ɗari da ashirin (120,000) marasa alhaki, da
kuma dabbobi masu yawa ba?”

# Mika

[1] Maganar UBANGIJI ta zo wa Mika mutumin Moreshet a zamanin Yotam, da na Ahaz, da kuma na Hezekiya, sarakunan Yahuda, Mika ya ga wahayi a kan Samariya da kuma a kan Urushalima. Ga abin da ya ce.

[2] Ku ji, ya ku mutane duka,
ki saurara, ya ke duniya da dukan mazauna cikinki,
bari UBANGIJI Mai Iko Duka yă zama shaida a kanku,
daga haikalinsa mai tsarki.

*Hukunci a kan Samariya da kuma Urushalima*

[3] Duba! UBANGIJI yana zuwa daga wurin zamansa;
zai sauko yă taka maɗaukakan wuraren duniya.
[4] Duwatsu za su narke a ƙarƙashin ƙafafunsa,
kamar kaki a gaban wuta,
kwaruruka kuma za su ɓace,
kamar ruwan da yake gangarowa daga tsauni.
[5] Duk wannan zai faru saboda laifin Yaƙub,
da kuma zunuban gidan Isra'ila ne.
Mene ne laifin Yaƙub?
Shin, ba Samariya ba ce?
Ina ne maɗaukakan wuraren Yahuda?
Shin, ba Urushalima ba ce?

[6] "Saboda haka zan mai da Samariya tarin juji,
wurin noman inabi.
Zan zubar da duwatsunta a cikin kwari
in kuma bar harsashin gininta a bayyane.
[7] Za a ragargaje dukan allolinta;
za a ƙone dukan baye-bayenta na haikali da wuta;
zan lalatar da dukan gumakanta.
Tun da ta wurin karuwanci ne ta tattara su,
ga karuwanci kuma za su koma."

*Kuka da Makoki*

[8] Saboda wannan zan yi baƙin ciki, in yi kuka;
zan yi tafiya ba takalmi, zan tuɓe, in kuma yi tafiya tsirara.
Zan yi kuka kamar dila,
in yi baƙin ciki kamar mujiya.
[9] Gama raunin Samariya ba mai warkewa ba ne;
ya bazu har Yahuda.
Ya ma kai bakin ƙofar mutanena,
har ma Urushalima da kanta.
[10] Kada a faɗe shi a Gat;*
kada ma a yi kuka.†
A maimako haka, a yi birgima a cikin ƙura
a Bet-Leyafra‡.

---

* **1:10** Gat ya yi kamar Ibraniyanci na faɗin wani abu. † **1:10** Da Ibraniyanci; Seftuwajin iya nufin ba a Akko ba ya yi kamar Ibraniyanci na kuka. ‡ **1:10** Bet Ofra yana nufin gidan laka.

11 Ku wuce tsirara da kuma kunya,
ku mazaunan Shafir§.
Bet-Ezel tana makoki
domin babu wani daga Za'anan*
da ya fito don yǎ taimaka.
12 Mazaunan Marot†
sun ƙosa su ga alheri,
amma UBANGIJI ya sauko da azaba,
har zuwa ƙofar Urushalima.
13 Ku da kuke zama a Lakish,‡
ku ɗaura wa dawakai kekunan yaƙi.
Gama ku kuka fara yin zunubi
a Sihiyona,
gama an sami laifofin Isra'ila
a cikinku.
14 Saboda haka za ku ba da kyautan bankwana
ga Moreshet Gat.
Garin Akzib§ zai zama abin yaudara
ga sarakunan Isra'ila.
15 Ku mazaunan Maresha*
UBANGIJI zai kawo wanda zai ci ku da yaƙi.
Sarakunan Isra'ila
za su gudu zuwa Adullam.
16 Ku aske kanku ƙwal don makoki,
ku yi wa kanku ƙwalƙwal kamar ungulu.
Gama za a ja 'ya'yan da kuke farin ciki
a kai su bauta.

# 2

### *Shirin mutum da na Allah*

1 Taku ta ƙare, ku da kuke shirya makirci,
ku da kuke ƙulle-ƙullen mugunta a kan gadonku!
Da gari ya waye sai ku fita ku aikata mugunta
domin ikon aikatawa yana hannunku.
2 Kukan yi ƙyashin gonaki ku kuma ƙwace su,
ku yi ƙyashin gidaje ku kuma ƙwace.
Kukan zalunci mutum, ku ƙwace masa gidansa,
har ku ƙwace masa gādonsa.
3 Saboda haka, UBANGIJI ya ce,
"Ina shirya wa waɗannan mutane bala'i,
yadda ba za ku iya ceton kanku ba.
Ba za ku ƙara tafiya kuna taƙama ba,
gama zai zama lokacin bala'i ne.
4 A wannan rana mutane za su yi muku ba'a
za su yi muku gwalo da wannan waƙar makoki,
'An lalatar da mu sarai;
an rarraba mallakar mutanena.
Ya ɗauke shi daga gare ni!

---

§ **1:11** Shafir yana nufin jin daɗi. * **1:11** Za'anan ya yi kamar Ibraniyanci na fito waje. † **1:12** Marot ya yi kamar Ibraniyanci na ɗaci ‡ **1:13** Lakish ya yi kamar Ibraniyanci na ƙungiya. § **1:14** Akzib yana nufin yaudara. * **1:15** Maresha ya yi kamar Ibraniyanci na mai nasara.

Ya miƙa filayenmu ga maciyan amanarmu.’ ”

5 Saboda haka ba za ku kasance da wani a taron jama’ar UBANGIJI
da zai raba ƙasar ta wurin jefa ƙuri’a ba.

*Annabawan ƙarya*

6 “Kada ku yi annabci” in ji annabawansu.
“Kada ku yi annabci game da waɗannan abubuwa;
abin kunya ba zai same mu ba.”
7 Daidai ne a ce, ya gidan Yaƙub,
“Ruhun UBANGIJI yana fushi ne?
Yana yin irin waɗannan abubuwa?”

“Ashe, maganata ba tă amfane
wanda ayyukansa suke daidai ba?
8 Ba da daɗewa ba mutanena sun tashi
kamar magabci.
Kun tuɓe riga mai tsada
daga waɗanda suke wucewa ba tare da kun damu ba,
sai ka ce mutanen da suke komowa daga yaƙi.
9 Kun kori matan mutanena
daga gidajensu masu daɗi.
Kuka kawar da albarkata har abada
daga wurin ’ya’yansu.
10 Ku tafi, ku ba ni wuri!
Gama wannan ba wurin hutunku ba ne,
gama ya ƙazantu,
ya zama kangon da ya wuce gyara.
11 In maƙaryaci da mazambaci ya zo ya ce,
‘Zan yi muku annabci ku sami wadataccen ruwan inabi da barasa,’
zai dai zama annabin da ya dace da wannan mutane ne!

*An yi alkawarin ’yantarwa*

12 “Tabbatacce zan tattara ku duka, ya gidan Yaƙub;
zan tattara ku raguwar Isra’ila.
Zan kawo su wuri ɗaya kamar
tumaki a cikin garke,
kamar garke a wajen kiwonsa;
wurin zai cika da mutane.
13 Wanda ya fasa ƙofa ya buɗe, shi zai haura yă yi musu jagora,
za su fashe bangon su fita.
Sarkinsu zai wuce gabansu,
UBANGIJI kuma zai kasance a gaba.”

# 3

*An Tsawata wa Shugabanni da Annabawa*

1 Sa’an nan na ce,
“Ku kasa kunne, ku shugabannin Yaƙub,
ku masu mulkin gidan Isra’ila.
Ya kamata ku san shari’a,
2 ku da kuke ƙin abu mai kyau kuke ƙaunar mugunta,
ku da kuke feɗe mutanena

kuke tuge nama daga ƙasusuwansu;
3 ku da kuke cin naman mutanena,
ku feɗe fatar jikinsu
kuke kakkarya ƙasusuwansu,
kuke yayyanka su gunduwa-gunduwa kamar naman da za a toya,
kamar naman da za a sa a dafa."

4 Sa'an nan za su kira ga UBANGIJI,
amma ba zai amsa musu ba.
A wannan lokaci zai ɓoye fuskarsa daga gare su
saboda irin muguntar da suka yi.
5 Ga abin da UBANGIJI ya faɗa,
"Game da annabawa
masu ɓad da mutanena,
in wani ya ciyar da su,
sai su ce akwai 'salama'
amma in bai ciyar da su ba,
a shirye suke su kai masa hari.
6 Saboda haka dare yana zuwa a bisanku, ba tare da wahayi ba,
kuma duhu, ba tare da duba ba.
Rana za tă fāɗi wa annabawa,
yini kuma zai zama musu duhu.
7 Masu gani za su ji kunya,
masu duba kuma za su ji taƙaici.
Dukansu za su rufe fuskokinsu
gama ba amsa daga Allah."
8 Amma game da ni, ina cike da iko
ta wurin Ruhun UBANGIJI
da kuma adalci da ƙarfi,
don a sanar da Yaƙub laifofinsa,
ga Isra'ila kuma zunubinsa.

9 Ku ji wannan, ku shugabannin gidan Yaƙub,
ku masu mulkin gidan Isra'ila,
ku da kuke ƙyamar gaskiya,
kuka karkatar duk abin da yake na gaskiya;
10 kuka gina Sihiyona ta wurin zub da jini,
Urushalima kuma ta wurin mugunta.
11 Hukunce-hukuncen shugabannin ƙasar na cin hanci ne,
firistocinta kuma suna koyarwa don a biya su,
annabawanta kuwa suna yin annabci don neman kuɗi.
Duk da haka suna jingina a kan UBANGIJI suna cewa,
"Ba UBANGIJI yana tare da mu ba?
Ba bala'in da zai zo mana."
12 Don haka, saboda ku,
za a nome Sihiyona kamar gona,
Urushalima kuma ta zama tarin juji,
tudun haikali kuwa zai zama kurmin ƙayayyuwa.

# 4

*Dutsen UBANGIJI*

1 A kwanakin ƙarshe

za a kafa dutsen haikalin Ubangiji
yǎ zama babba a cikin duwatsu.
Za a ɗaga shi sama da tuddai,
mutane kuma za su riƙa ɗunguma zuwa gare shi.
2 Al'ummai da yawa za su zo su ce,
"Ku zo, bari mu haura zuwa dutsen Ubangiji,
zuwa gidan Allah na Yaƙub.
Zai koya mana hanyoyinsa,
don mu yi tafiya cikin hanyoyinsa."
Doka za tǎ fita daga Sihiyona,
maganar Ubangiji kuma daga Urushalima.
3 Zai shari'anta tsakanin mutane
yǎ kuma sulhunta tsakanin manyan al'ummai nesa da kuma kusa.
Har su mai da takubansu su zama garemani,
māsunsu kuma su zama wuƙaƙen askin itace.
Al'umma ba za tǎ ɗauki takobi gāba da wata al'umma ba,
ko a yi horarwa don yaƙi.
4 Kowa zai zauna a tushen kuringar inabinsa
da tushen ɓaurensa,
kuma ba wanda zai tsoratar da su,
gama Ubangiji Maɗaukaki ne ya faɗa.
5 Dukan al'ummai za su iya tafiya
a cikin sunan allolinsu;
mu dai za mu yi tafiya a cikin sunan Ubangiji
Allahnmu har abada abadin.

*Shirin Ubangiji*

6 "A wannan rana," in ji Ubangiji,
"zan tattara guragu;
zan kuma tara masu zaman bauta,
da waɗanda na sa suka damu.
7 Zan mai da guragu su zama raguwa,
waɗanda aka kora, su zama al'umma mai ƙarfi.
Ubangiji zai yi mulkinsu a Dutsen Sihiyona
daga wannan rana da kuma har abada.
8 Game da ke, ya hasumiyar tsaron garke,
Ya mafaka* Diyar Sihiyona,
za a maido miki da mulkinki na dā,
sarauta kuma za tǎ zo wa Diyar Urushalima."

9 Don me yanzu kike kuka da ƙarfi,
ba ki da sarki ne?
Masu shawararki sun hallaka ne,
da zafi ya cika ki kamar mace mai naƙuda?
10 Ki yi birgima cikin zafin azaba, ya Diyar Sihiyona,
kamar macen da take naƙuda,
don yanzu dole ki bar birni
ki kafa sansani a filin Allah.
Za ki tafi Babilon;
a can za a kuɓutar da ki.
A can ne Ubangiji
zai fanshe ki daga hannun maƙiyanki.

* **4:8** Ko kuwa tudu

11 Amma yanzu al'ummai da yawa
suna gāba da ke.
Suna cewa, "Bari a ƙazantar da ita,
bari mu zuba wa Sihiyona ido."
12 Amma ba su san
tunanin UBANGIJI ba;
ba su fahimci shirinsa ba,
shi da ya tattara su kamar dammuna a masussuka.
13 "Ki tashi ki yi sussuka, ya Diyar Sihiyona,
gama zan ba ki ƙahonin ƙarfe;
zan ba ki kofatan tagulla
domin ki ragargaje al'ummai masu yawa."
Za ki ba UBANGIJI dukan dukiyarsu da suka tara ta hanyar zamba,
wadatarsu kuma ga Ubangiji dukan duniya.

# 5

*An yi alkawarin mai mulki daga Betlehem*

1 Ki tattara sojojinki, ya ke birnin mayaƙa,*
gama an kewaye mu da yaƙi.
Za su bugi kumatun mai mulkin
Isra'ila da sandar ƙarfe.

2 "Amma ke, Betlehem ta Efrata,
ko da yake ke ƙarama ce daga cikin zuriyarki† a Yahuda,
daga cikinki wani zai zo domina
wanda zai yi mulkin Isra'ila,
wanda asalinsa‡
tun fil azal ne."§

3 Saboda haka za a yashe Isra'ila
har sai wadda take naƙuda ta haihu
sauran 'yan'uwansa kuma sun dawo
su haɗu da Isra'ilawa.

4 Zai tsaya yă yi kiwon garkensa
da ƙarfin UBANGIJI,
cikin girman sunan UBANGIJI Allahnsa.
Za su kuma zauna lafiya, gama girmansa
za tă kai har ƙarshen duniya.

5 Zai kuma zama salamarsu.
Sa'ad da Assuriyawa suka kawo wa ƙasarmu hari
suka tattake kagarunmu,
za mu tā da makiyaya bakwai,
har ma shugabannin mutane takwas su yi gāba da su.
6 Za su yi mulkin* ƙasar Assuriya da takobi,
ƙasar Nimrod kuma da zaran takobi.†
Zai cece mu daga hannun Assuriyawa
sa'ad da suka kawo wa ƙasarmu hari

* **5:1** Ko kuwa Kara ƙarfin katangarki, ya katangan birni † **5:2** Ko kuwa masu mulki ‡ **5:2** Da Ibraniyanci fitowa daga § **5:2** Ko kuwa daga madawwamin kwanaki * **5:6** Ko kuwa ragargaza † **5:6** Ko kuwa Nimrod a bakin ƙofofinta

suka kuma tattake zuwa cikin iyakokinmu.

7 Raguwar Yaƙub za tă kasance
a tsakiyar mutane masu yawa
kamar raɓa daga UBANGIJI,
kamar yayyafi a kan ciyawa,
wanda ba ya jiran mutum
ko kuma yă dakata wa ɗan adam.
8 Raguwar Yaƙub za tă kasance tare da al'ummai,
a cikin mutane masu yawa,
kamar zaki a cikin sauran namun jeji,
kamar ɗan zaki cikin garken tumaki,
wanda yake tattaka yă kuma yi kaca-kaca da su sa'ad da yake ratsa a cikinsu,
ba kuwa wanda zai cece su.
9 Za a ɗaga hannunka cikin nasara a kan abokan gābanka,
za a hallaka maƙiyanka duka.
10 "A wannan rana," in ji UBANGIJI
"Zan hallaka dawakanku daga cikinku,
in kuma rurrushe kekunan yaƙinku.
11 Zan hallaka biranen ƙasarku
in yi rugu-rugu da dukan katangunku.
12 Zan kawar da maitarku,
ba za a ƙara yin sihiri ba.
13 Zan sassare dukan gumakan da kuka sassaƙa
da keɓaɓɓun duwatsunku a cikinku,
nan gaba ba za ku ƙara rusuna
wa aikin hannuwanku ba.
14 Zan tumɓuke daga gare ku ginshiƙan Asheranku‡
in kuma rurrushe biranenku.
15 Zan yi ramuwa cikin fushi da hasala
a kan al'umman da ba su yi mini biyayya ba."

# 6

## *Damuwar UBANGIJI a kan Isra'ila*

1 Ku saurari abin da UBANGIJI ya ce,
"Tashi ku gabatar da ƙararku a gaban duwatsu;
bari tuddai su ji abin da kuke so ku faɗa.

2 "Ku saurara, ya ku duwatsu game da tuhumar da UBANGIJI yake muku,
ku ji, ku daɗaɗɗun tushin duniya.
Gama UBANGIJI yana da ƙara a kan mutanensa;
yana tuhumar Isra'ila.

3 "Ya ku mutanena, me na yi muku?
Ta yaya na nawaita muku? Ku amsa mini.
4 Na fito da ku daga ƙasar Masar
na kuma 'yantar da ku daga ƙasar bauta.
Na aika da Musa yă jagorance ku,
haka ma Haruna da Miriyam.
5 Ya ku mutanena, ku tuna

‡ **5:14** Wato, alamar alliyar Ashera

abin da Balak sarkin Mowab ya ƙulla
da kuma amsar da Bala'am ɗan Beyor ya bayar.
Ku tuna da tafiyarku daga Shittim zuwa Gilgal,
don ku san ayyukan adalcin UBANGIJI."

6 Da me zan zo a gaban UBANGIJI
in rusuna a gaban Maɗaukaki Allah?
Shin, zan zo ne a gabansa da hadaya ta ƙonawa,
da ɗan maraƙi bana ɗaya?
7 UBANGIJI zai ji daɗin hadayar raguna dubbai
da kuma rafuffukan mai dubbai goma?
Zan ba da ɗan farina ne don laifina,
ko 'ya'yan jikina domin zunubin raina?
8 Ya nuna maka, ya mutum, abin da yake mai kyau.
Me UBANGIJI yake bukata daga gare ka kuwa
shi ne ka yi gaskiya ka so aikata jinƙai
ka kuma yi tafiya da tawali'u a gaban Allah.

*Laifin Isra'ila da kuma hukunci*

9 Ku saurara! UBANGIJI yana kira ga birni,
a ji tsoron sunana kuwa hikima ce,
"Ku kasa kunne ga sandan nan da kuma wannan wanda ya naɗa.*
10 Har yanzu zan manta, ya muguwar gida
da dukiyarki da kika samu a muguwar hanya
zan kuma manta da bugaggen mudun awo† wanda ake zargi?
11 Zan kuɓutar da mutumin da yake da ma'auni na rashin gaskiya,
da kuma buhun ma'aunan ƙarya?
12 Attajiranta masu fitina ne;
mutanenta kuma maƙaryata ne
harsunansu kuwa suna yaudara.
13 Saboda haka, zan hallaka ku
in lalace ku saboda zunubanku.
14 Za ku ci amma ba za ku ƙoshi ba,
cikinku zai zama babu kome‡
Za ku tattara amma ba za ku yi ajiyar kome ba,
gama abin da kuka yi ajiya zan ba wa takobi.
15 Za ku yi shuki amma ba za ku girba ba;
za ku matse zaitun amma ba za ku yi amfani da mai wa kanku ba,
za ku tattaka 'ya'yan inabi amma ba za ku sha ruwan inabin ba.
16 Kuna kiyaye ƙa'idodin Omri
da dukan ayyukan gidan Ahab
kun kuma bi al'adunsu.
Saboda haka, zan maishe ku kufai
in mai da ku abin dariya a cikin mutane,
za ku sha reni a wurin al'ummai."§

# 7

*Baƙin cikin Isra'ila*

---

* **6:9** Ma'anar Ibraniyanci na wannan layin babu tabbas. † **6:10** Efa mudun awo ne na busasshen abu. ‡ **6:14** Ma'anar Ibraniyanci na wannan kalma babu tabbas. § **6:16** Seftuwajin; da Ibraniyanci suna da abin zargi ga mutanena ne a nan

1 Tawa ta ƙare!
Ina kama da wanda yake tattara ʼyaʼyan itatuwa
a lokacin kalar ʼyaʼyan inabi;
babu sauran nonon inabin da za a tsinka a ci,
babu kuma ʼyaʼyan ɓaure na farko-farkon da raina yake marmari.
2 An kawar da masu tsoron Allah daga ƙasar;
babu sauran mai adalcin da ya rage.
Dukan mutane suna kwanto don su zub da jini;
kowa yana farautar ɗanʼuwansa da tarko.
3 Dukan hannuwansu sun gwaninta wajen yin mugunta;
shugabanni suna nema a ba su kyautai,
alƙalai suna nema a ba su cin hanci,
masu iko suna faɗar son zuciyarsu,
duk suna ƙulla makirci tare.
4 Mafi kyau a cikinsu yana kama da ƙaya,
mafi gaskiyarsu ya fi shingen ƙaya muni.
Ranar da Allah zai ziyarce ku ta zo,
ranar da masu gadinku za su hura ƙaho.
Yanzu ne lokacin ruɗewarku.
5 Kada ka yarda da maƙwabci;
kada ka sa begenka ga abokai.
Ko ma wadda take kwance a ƙirjinka,
ka yi hankali da kalmominka.
6 Gama ɗa yakan ce wannan ba mahaifinsa ba ne,
diya kuma takan tayar wa mahaifiyarta,
matar ɗa takan yi gāba da uwar mijinta,
abokan gāban mutum su ne iyalin cikin gidansa.

7 Amma game da ni, zan sa bege ga Ubangiji,
ina sauraron Allah Mai Cetona;
Allahna kuwa zai ji ni.

### *Israʼila za tă tashi*

8 Kada ku yi farin ciki, ku maƙiyana!
Ko da yake na fāɗi, zan tashi.
Ko da yake na zauna a cikin duhu,
Ubangiji zai zama haskena.
9 Domin na yi masa zunubi,
zan fuskanci fushin Ubangiji,
har sai ya dubi batuna
ya kuma tabbatar da ʼyancina.
Zai kawo ni zuwa wurin haske;
zan ga adalcinsa.
10 Saʼan nan maƙiyina zai gani
yă kuma sha kunya,
shi da yake ce da ni
"Ina Ubangiji Allahnka?"
Zai gani, yă kuma ji kunya.
Ko yanzu ma za a tattake shi
kamar taɓo a tituna.

11 Ranar gina katangarka tana zuwa,

a ranar za a fadada iyakokinka.
12 A wannan rana mutane za su zo gare ka
daga Assuriya da kuma biranen Masar,
daga Masar ma har zuwa Yuferites
daga teku zuwa teku,
kuma daga dutse zuwa dutse.
13 Duniya za tă zama kufai saboda mazaunanta,
saboda ayyukansu.

### *Addu'a da yabo*

14 Ka yi kiwon mutanenka da sandarka,
garken gādonka,
wanda yake zaune shi kaɗai a kurmi,
a ƙasa mai kyau ta kiwo,*
bari su yi kiwo a Bashan da Gileyad
kamar a kwanakin dā.

15 "Kamar a kwanakin da kuka fito daga Masar,
zan nuna musu al'ajabaina."

16 Al'ummai za su gani su kuma ji kunya,
za a kuma ƙwace musu dukan ikonsu.
Za su kama bakinsu
kunnuwansu kuma za su zama kurame.
17 Za su lashi ƙura kamar maciji,
kamar dabbobi masu rarrafe a ƙasa.
Za su fito daga maɓuyarsu da rawan jiki,
za su juya cikin tsoro ga UBANGIJI Allahnmu
su kuma ji tsoronku.
18 Wane ne Allah kamar ka,
wanda yake yafe zunubi yă kuma gafarta laifofin mutanensa da suka ragu?
Ba ka zama mai fushi har abada
amma kana marmari ka nuna jinƙai.
19 Za ka sāke jin tausayinmu;
za ka tattake zunubanmu a ƙarƙashin sawunka
ka kuma tura dukan kurakuranmu zuwa cikin zurfafan teku.
20 Za ka yi wa Yaƙub aminci,
ka kuma nuna jinƙai ga Ibrahim,
kamar yadda ka yi alkawari da rantsuwa ga kakanninmu
tun a kwanankin dā.

---

* **7:14** Ko kuwa a tsakiyar Karmel

# Nahum

[1] Jawabi game da Ninebe a littafin wahayin Nahum, mutumin Elkosh.

*Fushin UBANGIJI a kan Ninebe*

[2] UBANGIJI Allah mai kishi ne, mai sakayya kuma.
UBANGIJI Allah mai kishi ne, mai ɗaukar fansa kuma.
UBANGIJI yakan ɗauki fansa a kan maƙiyansa,
yakan ci gaba da fushi a kan abokan gābansa.
[3] UBANGIJI mai jinkirin fushi ne, mai iko duka kuma.
UBANGIJI ba zai bar masu zunubi babu horo ba.
Hanyarsa tana cikin guguwa da kuma hadari,
gizagizai kuwa su ne ƙurar ƙafafunsa.
[4] Yakan tsawata wa teku yă kuma busar da shi;
yakan sa dukan koguna su kafe.
Bashan da Karmel sun yi yaushi
tohon Lebanon kuma ya koɗe.
[5] Duwatsu suna rawan jiki a gabansa
tuddai kuma sun narke.
Duniya da dukan abin da yake cikinta
suna rawan jiki a gabansa.
[6] Wa zai iya tsaya wa fushinsa?
Wa yake da ikon jimre wa zafin hasalarsa?
Ana zuba fushinsa kamar wuta;
aka kuma ragargaza duwatsu a gabansa.

[7] UBANGIJI nagari ne,
mafaka kuma a lokacin wahala.
Yana kula da waɗanda suka dogara gare shi,
[8] amma da ambaliyar ruwa
zai kawo Ninebe ga ƙarshe;
zai fafari maƙiyansa zuwa cikin duhu.

[9] Dukan abin da suke ƙullawa game da UBANGIJI* zai kawo ga ƙarshe;
wahala ba za tă sāke komowa ƙaro na biyu ba.
[10] Za su sarƙafe a ƙaya,
za su kuma bugu da ruwan inabinsu;
za a laƙume su kamar busasshiyar ciyawa.†
[11] Daga cikinki, ya Ninebe wani ya fito
wanda ya ƙulla wa UBANGIJI makirci
yana ba da mugayen shawarwari.
[12] Ga abin da UBANGIJI ya ce,
"Ko da yake sun yi tarayya, suna kuma da yawa,
za a yanke su, a kawar a su.
Ko da yake na ba ki azaba, ya Yahuda,
ba zan ƙara ba ki azaba ba.
[13] Yanzu zan karya karkiyarsu daga wuyanki

* **1:9** Ko kuwa Mene ne ku maƙiya kuke ƙullawa a kan UBANGIJI? Shi † **1:10** ma'anar kalman nan Ibraniyanci babu tabbas.

in kuma tsittsinke sarƙar da suka ɗaura ki."

14 UBANGIJI ya ba da umarni game da ke Ninebe,
"Ba za ki sami zuriyar da za tă ci gaba da sunanki ba.
Zan rurrushe siffofin da kuka sassaƙa da kuma gumakan da kuka ƙera
gumakan da suke a cikin haikalin allolinku.
Zan shirya kabarinki,
domin ke muguwa ce."

15 Duba, can a bisa duwatsu,
ga ƙafafu mai kawo labari mai daɗi,
wanda yake shelar salama!
Ki yi bukukkuwanki, ya Yahuda,
ki kuma cika wa'adodinki.
Mugaye ba za su ƙara mamaye ki ba;
domin za a hallaka su ƙaƙaf.

# 2

*Ninebe za tă fāɗi*

1 Mai hari yana matsowa a kanki, Ninebe.
Ki tsare mafaka,
ki yi gadin hanya
ki sha ɗamara
ki tattaro dukan ƙarfinki!

2 UBANGIJI zai maido da darajar Yaƙub,
kamar ta Isra'ila,
ko da yake masu washewa sun washe su
suka kuma lalatar da inabinsu.

3 Garkuwoyin sojojinsa ja wur ne;
jarumawansa suna sanye da kaya masu ruwan jan garura.
Karafan kekunan yaƙi suna walƙiya
a ranar da aka shirya su;
ana kaɗa māsu da bantsoro.*
4 Kekunan yaƙi sun zabura a tituna,
suna kai da kawowa a dandali.
Suna walƙiya kamar tocila
suna sheƙawa a guje kamar walƙiya.

5 Ninebe ta tattara rundunarta,
duk da haka sun yi ta tuntuɓe a kan hanyarsu.
Sun ruga zuwa katangan birnin,
sun sanya garkuwar kāriya a inda ya kamata.
6 An buɗe ƙofofin rafuffukan
sai wurin ya rurrushe.
7 An umarta† cewa birnin
za tă tafi bauta, za a kuma yi gaba da su.
Bayi 'yan mata suna kuka kamar tattabaru
suna buga ƙirjinsu.

* 2:3 Da Ibraniyanci; Seftuwajin da Siriyak / mahayan dawakai suna kai da kawowa † 2:7 Ma'anar kalmar da Ibraniyanci babu tabbas.

8 Ninebe tana kama da tafki,
wanda ruwanta yana yoyo.
Suna kuka suna cewa, “Ku tsaya! Ku tsaya,”
amma ba wanda ya waiga.
9 A washe azurfa;
a washe zinariya;
dukiyarsu ba ta da iyaka,
arzikinsu kuma ba ya ƙarewa.
10 Ta zama wofi, an washe ta, an tuɓe ta!
Zukata sun narke, gwiwoyi suna kaɗuwa,
jikuna suna rawa, fuskoki duk sun kwantsare!

11 Ina kogon zakokin nan yake yanzu,
inda suka ciyar da ʼyaʼyansu,
inda zaki da zakanya sukan shiga,
da ʼyaʼyansu, ba mai damunsu
12 Zaki ya kashe abin da ya ishe ʼyaʼyansa
ya kuma murɗe wuyan dabbobi
ya cika wurin zamansa da abin da ya kama
ya cika kogwanninsa da abin da ya kashe.

13 “Ina gāba da ke,”
in ji Ubangiji Maɗaukaki.
“Zan ƙone kekunan yaƙinki,
takobi kuma zai fafare ʼyaʼyan zakokinki.
Ba kuma zan bar miki namun jejin da za ki kashe a duniya ba.
Ba kuwa za a ƙara jin
muryar ʼyan saƙonki ba.”

# 3

### *Kaiton Ninebe*

1 Kaiton birni mai zub da jini,
wadda take cike da ƙarairayi,
cike da ganima,
wadda ba a rasa masu fāɗawa cikin wahala!
2 Ku ji karar bulala
da kwaramniyar ƙafafu,
da sukuwar dawakai
da girgizar kekunan yaƙi!
3 Mahaya dawakai sun kunno kai,
takuba suna walƙiya,
māsu kuma suna ƙyali;
ga ɗumbun da aka kashe
ga tsibin matattu,
gawawwaki ba iyaka,
mutane suna tuntuɓe da gawawwaki,
4 duk saboda yawan shaʼawace-shaʼawacen karuwa,
mai daɗin baki, uwargidan maita,
wadda ta ɓad da alʼummai ta wurin karuwancinta
ta kuma ɓad da mutane ta wurin maitancinta.

5 “Ina gāba da ke,” in ji UBANGIJI Maɗaukaki.
“Zan kware fatarinki a idonki.
Zan nuna wa al’ummai tsiraicinki,
masarautai kuma kunyarki.
6 Zan watsa miki ƙazanta,
in yi miki wulaƙanci
in kuma mai da ke abin reni.
7 Duk wanda ya gan ki zai gudu daga gare ki yana cewa,
‘Ninebe ta lalace, wa zai yi makoki domin ta?’
Ina zan sami wani wanda zai yi miki ta’aziyya?”

8 Kin fi Tebes* ne
da take a bakin Nilu,
da ruwa yake kewaye da ita?
Rafi shi ne kāriyarta,
ruwanta kuma katanga.
9 Kush† da kuma Masar su ne ƙarfinta marar iyaka;
Fut da Libiya suna cikin mataimakanta.
10 Duk da haka an tafi da ita
ta kuma tafi bauta.
Aka fyaɗa ƙananata da ƙasa
aka yayyanka su gunduwa-gunduwa a kan kowane titi.
Aka jefa ƙuri’a a kan manyan mutanenta,
aka daure manyan mutanenta da sarƙoƙi.
11 Ke ma za ki bugu,
za ki ɓuya.
Ki kuma nemi mafaka daga wurin abokin gāba.

12 Dukan kagarunki suna kama da itatuwan ɓaure
da ’ya’yansu da suka nuna.
Da an girgiza,
sai ɓaure su zuba a bakin mai sha.
13 Dubi mayaƙanki,
duk mata ne!
Kofofin ƙasarki
a buɗe suke ga abokan gābanki,
wuta ta cinye madogaransu.

14 Ki ja ruwa gama za a kewaye ki da yaƙi.
Ki ƙara ƙarfin kagaranki!
Ki kwaɓa laka,
ki sassaƙa turmi
ki gyara abin yin tubali!
15 A can wuta za tă cinye ki;
takobi zai sare ki,
kuma kamar fāra, za a cinye ki.
Ki riɓaɓɓanya kamar fāra,
ki riɓaɓɓanya kamar fārin ɗango!
16 Kin ƙara yawan masu kasuwancinki
har sai da suka fi taurarin sama.
Amma kamar fāra sun cinye ƙasar

---

* 3:8 Ibraniyanci Ba Amon † 3:9 Wato, yankin Nilu na Bisa

sa’an nan suka tashi, suka tafi.
17 Masu tsaronki suna kama da fāri ɗango,
shugabanninki sun yi cincirindo kamar fārin ɗango
da suka sauka a kan bango a rana mai sanyi,
amma da rana ta fito, duk za su tashi su tafi,
ba kuma wanda ya san inda suka nufa.

18 Ya sarkin Assuriya, makiyayanka‡ sun yi barci;
manyan mutanenka sun kwanta su huta.
An watsar da mutanenka a cikin duwatsu,
ba wanda zai tattaro su.
19 Ba abin da zai warkar da rauninka;
rauninka ya yi muni.
Duk wanda ya ji labarinka
zai tafa hannuwansa saboda farin cikin fāɗuwarka,
gama wane ne bai ji
jiki a hannunka ba?

‡ **3:18** Ko kuwa masu mulki

# Habakkuk

1 Saƙon da annabi Habakkuk ya karɓa.

*Habakkuk ya nuna damuwa*

2 Har yaushe, ya UBANGIJI, zan yi kukan neman taimako,
amma ka ƙi ji?
Ina kuka a gare ka saboda zalunci
amma ba ka ce ufam ba.
3 Me ya sa ka bari ina ta kallon rashin gaskiya?
Me ya sa kake barin abin da ba daidai ba?
Hallaka da tashin hankali suna a gabana;
ga rashin jituwa da faɗa ko'ina.
4 Saboda haka ba a bin doka,
shari'a kuma ba ta aiki.
Mugaye sun kewaye masu adalci
don a hana gaskiya tă yi aiki.

*Amsar UBANGIJI*

5 "Ka dubi al'ummai, ka gani,
ka sha mamaki.
Ga shi zan yi wani abu a kwanakinka,
wanda ko ma an faɗa maka
ba za ka gaskata ba.
6 Zan tā da Babiloniyawa,*
waɗannan marasa hankali da kuma marasa tausayi; masu gajeren haƙuri,
waɗanda suke ratsa ko'ina a duniya
don su ƙwace wuraren zaman da ba nasu ba.
7 Suna da bantsoro da firgitarwa;
dokoki da ƙa'idodinsu ne
kawai suka sani.
8 Dawakansu sun fi damisoshi sauri,
sun fi kyarketan yamma zafin rai.
Mahayansu suna zuwa a guje;
mahayansu daga nesa suka fito.
Suna firiya kamar ungulu mai sauka da gaggawa don yă ci mushe;
9 duk sukan zo da nufin tā-da-na-zaune-tsaye.
Ana jin tsoronsu tun ma kafin su iso
suna tattara bayi kamar yashi.
10 Sukan yi wa sarakuna ba'a
su kuma rena masu mulki.
Sukan yi wa dukan birane masu mafaka dariya;
sukan tara ƙasa su hau, su cinye abokan gābansu da yaƙi.
11 Sa'an nan su wuce da sauri kamar iska,
mutane ne masu laifi, waɗanda ƙarfinsu shi ne allahnsu."

*Damuwa ta biyu ta Habakkuk*

12 Ya UBANGIJI, ba tun fil azal kake ba?
Ya Allahna, Mai Tsarkina, ba za mu mutu ba.
Ya UBANGIJI ka sanya su su tabbatar da hukunci;

* **1:6** Ko kuwa Kaldiyawa

Ya Dutse, ka naɗa su don su yi hukunci.
13 Idanunka masu tsarki ne da suka fi gaban duban mugunta;
ba ka amince da abin da ke ba daidai ba.
To, don me ka ƙyale munafukai suna cin karensu ba babbaka?
Me ya sa kake shiru sa'ad da mugaye
suke haɗiye adalai da suka fi su adalci?
14 Ka mai da maza kamar kifin teku,
kamar halittun tekun da ba su da shugaba.
15 Mugu abokin gāba yakan kama su duka da ƙugiya,
yă jawo su waje da abin kamun kifinsa,
yă tattara su cikin ragarsa,
ta haka yakan yi murna da farin ciki.
16 Saboda haka yakan yi hadaya wa abin kamun kifinsa
yă kuma ƙona turare wa ragarsa,
domin ta wurin abin kamun kifinsa ne yake yin rayuwar jin daɗi
yă kuma zaɓi irin abincin da yake so.
17 Zai ci gaba da juye abin kamun kifinsu ke nan,
suna hallaka al'ummai ba tausayi?

# 2

1 Zan tsaya wurin tsarona
in kuma zauna a kan katanga;
zan jira in ga abin da zai ce mini,
da kuma wace amsa zan bayar ga wannan kuka.

*Amsar Ubangiji*

2 Sa'an nan Ubangiji ya amsa ya ce,
"Ka rubuta wannan ru'uya
ka bayyana ta a fili a kan alluna
don mai shela* yă ruga da ita, yă kai.
3 Gama ru'uyar tana jiran ƙayyadadden lokaci;
tana zancen ƙarshe
kuma ba za tă zama ƙarya ba.
Ko da ka ga kamar tana jinkiri, ka jira ta;
lalle za tă† zo, ba za tă makara ba.

4 "Duba, abokin gāba ya cika da ɗaga kai;
sha'awarsa ba daidai ba ce,
amma mai adalci zai rayu ta wurin bangaskiyarsa‡,
5 ba shakka, ruwan inabi ya yaudare shi;
yana fariya kuma ba ya hutu.
Domin shi mai haɗama ne kamar kabari§
kuma kamar mutuwa, ba ya ƙoshi;
yakan tattara dukan al'ummai wa kansa
yana kuma kama dukan mutane su zama kamammu.
6 "Dukansu ba za su yi masa tsiya, suna yin masa ba'a da dariya ba, suna cewa,
" 'Kaito ga wannan wanda ya tara wa kansa kayan sata

* **2:2** Ko kuwa duk wanda ya karanta † **2:3** Ko kuwa ko da yake ya daɗe, ka jira shi ‡ **2:4** Ko kuwa amintacce
§ **2:5** Da Ibraniyanci Sheol

ya kuma wadatar da kansa da kayan ƙwace!
Har yaushe wannan abu zai ci gaba?'
7 Masu binka bashi* ba za su taso maka nan da nan ba?
Ba za su farka su sa ka fargaba ba?
Ta haka ka zama ganima a gare su.
8 Domin ka washe al'ummai masu yawa,
mutanen da suka rage za su washe ka.
Domin ka zub da jinin mutane;
ka hallaka ƙasashe, da birane, da kuma kowa da yake cikinsu.

9 "Kaito ga wanda ya gina masarautarsa da ƙazamar riba
don yǎ kafa sheƙarsa can bisa,
don yǎ tsere wa zama kango!
10 Ka ƙulla lalacin mutane masu yawa,
ta haka ka kunyatar da gidanka ka kuma hallaka ranka.
11 Duwatsun katanga za su yi kuka,
ginshiƙan katako kuma za su amsa.

12 "Kaiton mutumin da ya gina birni da jinin da ya zubar
ya kuma kafa gari ta wurin mugun aiki!
13 Ba UBANGIJI Maɗaukaki ne ya ƙudura
cewa wahalar mutane ta zama mai kawai don wuta ba,
cewa al'ummai su gajiyar da kansu a banza ba?
14 Gama duniya za tǎ cika da sanin ɗaukakar UBANGIJI,
yadda ruwaye suka rufe teku.

15 "Kaito wanda ya ba wa maƙwabtansa abin sha,
yana ta zubawa daga salkan ruwan inabi har sai sun bugu,
don dai yǎ ga tsiraicinsu.
16 Za ka cika da kunya a maimakon ɗaukaka.
Yanzu lokacinka ne! Kai ma ka sha, a kuma tone asirinka!†
Gama kwaf na hannun daman UBANGIJI yana zuwa kewaye da kai,
abin kunya kuma zai rufe darajarka.
17 Ɓarnar da ka yi wa Lebanon zai komo kanka,
kuma hallakar dabbobin da ka yi zai sa dabbobi su tsorata ka.
Gama ka zub da jinin mutum;
ka hallaka ƙasashe, da birane, da kuma kowa da yake cikinsu.

18 "Ina amfanin gunki da mutum ne ya sassaƙa?
Ko siffar da take koyar da ƙarya?
Gama wanda ya yi shi yana dogara ne ga halittarsa;
ya yi gumakan da ba sa magana.
19 Kaito wanda ya ce da katako, 'Rayu!'
Ko kuwa dutse marar rai, 'Farka!'
Zai iya bishewa ne?
An dalaye shi da zinariya da azurfa;
ba numfashi a cikinsa."

20 Amma UBANGIJI yana a cikin haikalinsa mai tsarki;

* **2:7** Ko kuwa mai bin bashi † **2:16** Masoretik; Mataccen Teku, Akwila, Bulget da Siriyak (duba kuma Seftuwajin) da kuma tangaɗi

bari dukan duniya tă yi shiru a gabansa.

# 3

*Addu'ar Habakkuk.*

1 Addu'ar annabi Habakkuk. A kan *shigiyont*.*
2 Ya UBANGIJI, na ji irin shaharar da ka yi;
na yi al'ajabi game da ayyukanka, ya UBANGIJI.
Ka maimaita su a kwanakinmu,
ka sanar da su a lokacinmu;
ka yi jinƙai ko a lokacin da kake fushi.

3 Allah ya zo daga Teman,
Mai Tsarkin nan daga Dutsen Faran.
Sela
†
Ɗaukakarsa ta rufe sammai
yabonsa kuma ya cika duniya.
4 Darajarsa ta yi kamar fitowar rana;
ƙyalƙyali ya wulga daga hannunsa,
inda ikonsa yake a ɓoye.
5 Annoba ta sha gabansa;
cuta kuma tana bin bayansa.
6 Ya tsaya, ya kuwa girgiza duniya;
ya duba, sai ya sa al'ummai suka yi rawan jiki.
Tsofaffin duwatsu sun wargaje
daɗaɗɗun tuddai kuma suka rurrushe.
Hanyoyinsa dawwammamu ne.
7 Na ga tentin Kushan cikin azaba;
wuraren zaman Midiyan cikin damuwa.

8 Ka ji haushin koguna ne, ya UBANGIJI?
Ko kuwa ka hasala da rafuffuka ne?
Ko ka yi fushi da teku ne
sa'ad da ka hau dawakanka
da kuma kekunan yaƙinka masu nasara?
9 Ka ja bakanka,
ka nemi a ba ka kibiyoyi masu yawa.
Sela
Ka raba duniya da koguna;
10 duwatsu sun gan ka sai suka ƙame.
Ruwaye masu hauka sun yi ta fantsamawa;
zurfafa suka yi ruri
suka tā da raƙuman ruwansu sama.

11 Rana da wata suka tsaya cik a sammai
da ganin kibiyoyinka masu wucewa fyu,
da ganin hasken māshinka mai walƙiya.
12 Cikin hasala ka ratsa duniya
cikin fushi kuma ka tattake ƙasashe.
13 Ka fito don ka fanshi mutanenka,

* **3:1** Mai yiwuwa a zahiri, ko kuma kalma ce ta waƙa † **3:3** kalma ce da babu tabbas; mai yiwuwa kalma ce ta waƙa; haka ma a ayoyin 9 da 13.

don ceci shafaffenka.
Ka ragargaza shugaban ƙasar mugaye,
ka tuɓe shi daga kai har ƙafa.

Sela

14 Da māshinsa ka soki kansa
sa'ad da jarumawansa suka fito don su tarwatse mu,
suna farin ciki sai ka ce masu shirin cinye
matalautan da suke a ɓoye.
15 Ka tattake teku da dawakanka,
kana kaɗa manyan ruwaye.

16 Na ji sai zuciyata ta buga,
leɓunana sun yi rawa da jin murya;
ƙasusuwana suka ruɓe,
ƙafafuna kuma sun yi rawa.
Duk da haka zan jira da haƙuri ga ranar bala'i
ta zo a kan al'umman nan mai kawo mana hari.
17 Ko da yake itace ɓaure bai tohu ba,
ba kuma 'ya'ya a kuringar inabi,
ko da yake zaitun bai ba da amfani ba,
gonaki kuma ba su ba da abinci ba,
ko da yake babu tumaki a garke,
ba kuma shanu a turaku,
18 duk da haka zan yi farin ciki da UBANGIJI,
zan yi murna da Allah Mai Cetona.

19 UBANGIJI Mai Iko Duka shi ne ƙarfina;
yakan mai da ƙafafuna kamar na barewa,
yakan sa in yi tafiya a wurare masu tsayi.
Domin mai bi da kaɗe-kaɗe. A kan kayan kiɗi masu tsirkiyata.

# Zefaniya

[1] Maganar UBANGIJI da ta zo wa Zefaniya ɗan Kushi, ɗan Gedaliya, ɗan Amariya, ɗan Hezekiya, a zamanin Yosiya ɗan Amon sarkin Yahuda.

*Gargaɗi a kan hallaka mai zuwa*

2 “Zan hallaka kome
a fuskar duniya,”
in ji UBANGIJI.
3 “Zan hallaka mutane da dabbobi;
zan kuma hallaka tsuntsayen sama
da kifayen teku,
da gumakan da suke sa mugaye su yi tuntuɓe.”*

“Sa’ad da zan kawar da mutum daga fuskar duniya,”
in ji UBANGIJI.
4 “Zan miƙa hannuna gāba da Yahuda
da kuma dukan mazaunan Urushalima.
Zan datse raguwar Ba’al daga wannan wuri,
da sunayen firistocin gumaka da na marasa sanin Allah,
5 waɗanda suka rusuna a kan rufin ɗaki
don su yi sujada ga rundunar taurari.
Waɗanda suka rusuna suka kuma yi rantsuwa da sunan UBANGIJI
suke kuma rantsuwa da sunan Molek.†
6 Waɗanda suka juya daga bin UBANGIJI,
ba sa kuma neman UBANGIJI ko su nemi nufinsa.”

7 Ku yi shiru a gaban UBANGIJI Mai Iko Duka,
gama ranar UBANGIJI ta yi kusa.
UBANGIJI ya shirya hadaya;
ya kuma tsarkake waɗanda ya gayyato.

8 “A ranar hadayar UBANGIJI
zan hukunta sarakuna
da kuma ’ya’yan sarakuna
da duk waɗanda suke sanye
da rigunan ƙasashen waje.
9 A wannan rana zan hukunta
dukan waɗanda suke kauce taka madogarar ƙofa,‡
waɗanda suke cika haikalin allolinsu
da rikici da ruɗu.

10 “A wannan rana,”
in ji UBANGIJI,
“Za a ji kuka daga Kofar Kifi,
kururuwa daga Sabon Mazauni,
da kuma amo mai ƙarfi daga tuddai.

---

* **1:3** Ma’anar Ibraniyancin nan babu tabbas. † **1:5** Da Ibraniyanci Malkam, wato, Milkom. ‡ **1:9** Dubi 1Sam 5.5.

11 Ku yi kururuwa, ku da kuke zaune a yankin kasuwa;§
za a hallaka dukan ʼyan kasuwanku,
dukan waɗanda suke kasuwanci da azurfa za su lalace.
12 A wannan lokaci zan bincike Urushalima da fitilu
in kuma hukunta waɗanda ba su kula ba,
waɗanda suke kamar ruwan inabin da aka bar a ƙasan tukunya,
waɗanda suke tsammani, ‘Ubangiji ba zai yi kome ba
nagari ko mummuna.’
13 Za a washe dukiyarsu,
a rurrushe gidajensu.
Za su gina gidaje
amma ba za su zauna a ciki ba;
za su shuka inabi
amma ba za su sha ruwansa ba.”

14 Babbar ranar Ubangiji ta yi kusa,
ta yi kusa kuma tana zuwa da sauri.
Ku saurara! Kukan ranar Ubangiji za tă yi zafi,
za a ji kururuwan jarumi a can.
15 Ranan nan za tă zama ranar fushi,
rana ce ta baƙin ciki da azaba,
rana ce ta tashin hankali da lalacewa,
ranar duhu baƙi ƙirin,
ranar gizagizai da baƙin duhu,
16 rana ce ta busa ƙaho da kururuwar yaƙi
gāba da birane masu mafaka,
da kuma kusurwar hasumiyoyi.

17 “Zan kawo baƙin ciki a kan mutane
za su kuma yi tafiya kamar makafi,
domin sun yi wa Ubangiji zunubi.
Za a zubar da jininsu kamar ƙura
kayan cikinsu kuma kamar najasa.
18 Azurfarsu ko zinariyarsu
ba za su iya cetonsu ba
a ranar fushin Ubangiji.”

A cikin zafin kishinsa
za a hallaka dukan duniya
gama zai kawo ƙarshen dukan mazaunan duniya
nan da nan.

# 2

1 Ku tattaru, ku tattaru,
Ya ku alʼumma marar kunya,
2 kafin ƙayyadadden lokacin nan yă zo
ranan nan kuma ta share ku kamar ƙaiƙayi
kuma kafin fushi mai tsanani na Ubangiji yă auko muku,
kafin ranar fushin Ubangiji ta auko muku.
3 Ku nemi Ubangiji, dukanku ƙasashe masu tawaliʼu,

---
§ **1:11** Ko kuwa Turmi

ku da kuke yin abin da ya umarta.
Ku nemi adalci da tawali'u;
mai yiwuwa ku sami mafaka a ranar fushin UBANGIJI.

*Hukunci a kan Filistiya*

4 Za a yashe Gaza
a kuma bar Ashkelon kango.
Da tsakar rana Ashdod za tă zama babu kowa
a kuma tumɓuke Ekron.
5 Taku ta ƙare ku da kuke zama a bakin teku,
Ya ku mutanen Keretawa;
maganar UBANGIJI tana gāba da ke,
Ya ke Kan'ana, ƙasar Filistiyawa.
"Zan hallaka ki
kuma babu abin da zai rage."
6 Kasar da take a bakin teku, inda Keretawa* suke zaune,
za tă zama wurin da makiyaya da ta garken tumaki.
7 Za tă zama mallakar raguwar gidan Yahuda;
a can za su sami wurin kiwo.
Da yamma za su kwanta
a gidajen Ashkelon.
UBANGIJI Allahnsu zai lura da su;
zai maido musu da martabarsu.†

*Hukunci a kan Mowab da Ammon*

8 "Na ji irin zagin da Mowab take yi,
da kuma ba'ar Ammonawa,
waɗanda suka zagi mutanena
suna kuma yi barazana a kan ƙasarsu.
9 Saboda haka, muddin ina raye,"
in ji UBANGIJI Maɗaukaki,
Allah na Isra'ila,
"tabbatacce Mowab za tă zama kamar Sodom,
Ammonawa kuma kamar Gomorra,
ƙasa mai ciyayi da rammukan gishiri,
ƙasa marar amfani har abada.
Raguwar mutanena za su washe su;
waɗanda suka rage na al'ummata za su gāda ƙasarsu."

10 Wannan ne zai zama sakamakon girmankansu,
saboda zagi da kuma ba'ar da suka yi wa mutanen UBANGIJI Maɗaukaki.
11 UBANGIJI zai zama abin tsoro a gare su
sa'ad da ya hallaka allolin ƙasar.
Al'ummai a kowane bakin teku za su yi masa sujada,
kowa a ƙasarsa.

*Hukunci a kan Kush*

12 "Ku ma, ya Kushawa,‡
za a kashe ku da takobina."

*Hukunci a kan Assuriya*

13 Zai kuma miƙa hannunsa gāba da arewa

---

* **2:6** Ma'anar Ibraniyanci na wannan kalma ba ta da tabbas † **2:7** Ko kuwa zai dawo musu da waɗanda aka kwasa zuwa bauta ‡ **2:12** Wato, mutanen da suke a yankin kogin Nilu na Bisa

yă kuma hallaka Assuriya,
zai mai da Ninebe kango gaba ɗaya
ta kuma zama busasshiya kamar hamada.
14 Garkuna za su kwanta a can,
da kowace irin halitta,
Mujiyar hamada da bushiya
za su zauna a kan ginshiƙanta.
Kukansu za tă ratsa tagogi,
ɓuraguzai za su tare ƙofofin shiga,
za a kware ginshiƙan al'ul.
15 Birnin da yake harka ke nan
da take zaune lafiya.
Ta ce wa kanta,
"Ni ce, kuma babu kamata."
Dubi irin kangon da ta zama mana,
mazaunin namun jeji!
Duk wanda ya wuce ta sai ya yi mata tsaki
yana kaɗa kai.

## 3

*Nan gaba na Urushalima*

1 Taki ta ƙare, ke birnin mai danniya,
mai 'yan tawaye da kuma masu ƙazanta!
2 Ba kya yi wa kowa biyayya,
ba kya kuma yarda da kuskurenki.
Ba kya dogara ga Ubangiji,
ba kya kuma kusatowa kusa da Allahnki.
3 Sarakunanki ruri ne na zakoki,
shugabanninki kyarketan dare ne,
waɗanda ba sa rage kome don safe.
4 Annabawanki mahaukata ne
mutanenki masu cin amana ne.
Firistocinki suna ƙazantar da Wurin Mai Tsarki
suna kuma keta dokoki.
5 Ubangiji da yake cikinki mai adalci ne;
ba ya yin abin da ba daidai ba.
Kowace safiya yakan bayyana dokokinsa a fili,
kowace sabuwar rana kuma ba ya kāsawa,
duk da haka marasa adalci ba sa jin kunya.
6 "Na daddatse al'ummai;
an kuma rurrushe kagararsu.
Na bar titunansu ba kowa,
ba mai ratsawa a ciki.
An ragargaza biranensu;
ba wanda za a bari, babu ko ɗaya.
7 Na ce wa birnin,
'Tabbatacce za ki ji tsorona
ki kuma yarda da gyara!'
Ta haka ba za a datse wurin zamanki ba,
ba kuwa dukan hukuncena za su hau bisa kansu ba.
Amma har yanzu suna marmari
su yi rashin gaskiya a duk abin da suke yi.

8 Saboda haka ku jira ni,” in ji UBANGIJI;
“a ranar da zan tsaya in ba da shaida,*
Na yanke shawara in tattara dukan al’ummai,
in tattara mulkoki
in kuma zuba fushina a kansu,
da dukan zafin haushina.
Za a mamaye dukan duniya
da zafin fushina.

9 “Sa’an nan zan tsarkake leɓunan mutanen,
don dukansu su kira bisa ga sunan UBANGIJI
su kuma yi masa hidima kafaɗa da kafaɗa.
10 Tun daga ƙetaren rafuffukan Kush†
masu yi mini sujada, mutanena da suke a warwatse,
za su kawo mini hadayu.
11 A wannan rana ba za ku sha kunya
saboda laifofin da kuka yi mini,
gama zan ɗauke wa wannan birni
waɗanda suke farin ciki cikin girmankansu.
Ba kuma za ka ƙara yin kallon reni
a tuduna mai tsarki ba.
12 Amma zan zauna a cikinki
masu tawali’u da masu ƙasƙantar da kai,
waɗanda suke dogara ga sunan UBANGIJI.
13 Raguwar Isra’ila ba za su ƙara aikata abin da ba daidai ba,
ba za su faɗa ƙarya ba,
ba kuwa za a sami ruɗu a bakunansu ba.
Za su ci su kuma kwanta
kuma babu wanda zai ba su tsoro.”

14 Ki rera, ya Diyar Sihiyona;
ki tā da murya, ya Isra’ila!
Ki yi murna ki kuma yi farin ciki da dukan zuciyarki,
Ya Diyar Urushalima!
15 UBANGIJI ya ɗauke hukuncinki,
ya mai da abokan gābanki baya.
UBANGIJI, Sarkin Isra’ila, yana tare da ke;
ba kuma za ki ƙara jin tsoron wani lahani ba.
16 A wannan rana za su cewa Urushalima,
“Kada ki ji tsoro, ya Sihiyona;
kada ki bar hannuwanki su raunana.
17 UBANGIJI Allahnki yana tare da ke,
mai iko ne don ceto.
Zai yi matuƙar farin ciki da ke,
zai rufe ki da ƙaunarsa,
zai yi farin ciki da ke ta wurin rerawa.”

18 “Zan cire taƙaici daga gare ki
a ƙayyadaddun bukukkuwa;
su kaya ne da kuma zargi a gare ki.‡

* **3:8** Seftuwajin da Siriyak; Ibraniyanci zai tashi don yă washe † **3:10** Wato, yankin Nilu na Bisa ‡ **3:18** Ko kuwa “Zan tattara ku da kuke makoki domin ƙayyadaddun hidima; zarginki kaya ne a gare ni”

19 A wannan lokaci zan jijji wa
waɗanda suka danne ku;
zan kuɓutar da guragu
in kuma tattara waɗanda suke a warwatse.
Zan sa a yabe su a kuma girmama su
a kowace ƙasar da aka kunyatar da su.
20 A wannan lokaci zan tattara ku;
a wannan lokaci zan kawo ku gida,
zan sa a yabe ku a kuma girmama ku
a cikin dukan mutanen duniya
a sa'ad da na maido da arzikinku§
a idanunku,"
in ji UBANGIJI.

§ **3:20** Ko kuwa zan dawo da kamammunku

# Haggai

*Kira don gina gidan Ubangiji*

1 A shekara ta biyu ta mulkin Sarki Dariyus, a rana ta fari ga watan shida, maganar
Ubangiji ta zo ta wurin annabi Haggai zuwa ga Zerubbabel ɗan Sheyaltiyel, gwamnan
Yahuda, da kuma Yoshuwa ɗan Yehozadak, babban firist.
2 Ga abin da Ubangiji Maɗaukaki ya ce, “Waɗannan mutane sun ce, ‘Lokaci bai yi
ba tukuna da za a gina gidan Ubangiji.’ ”
3 Sa’an nan maganar Ubangiji ta zo ta wurin annabi Haggai cewa, 4 “Ashe, lokaci
ya yi da za ku zauna a ɗakunan da kuka yi da rufin katako, amma haikalin nan yana
zaman kufai?”
5 To, ga abin da Ubangiji Maɗaukaki ya ce, “Ku lura da al’amuranku. 6 Kun shuka
da yawa, amma kun girbe kaɗan. Kun ci, amma ba ku ƙoshi ba. Kun sha, amma ba
ku kashe ƙishirwa ba. Kun sa tufafi, amma ba ku ji ɗumi ba. Kuna karɓar albashi,
ya zama sai ka ce kuna zuba a hudajjen aljihu.”
7 Ga abin da Ubangiji Maɗaukaki ya ce, “Ku lura da al’amuranku. 8 Ku haura zuwa
kan duwatsu ku sauko da katakai don ku gina gidan, don ni ma in ji daɗinsa, in kuma
sami ɗaukaka,” in ji Ubangiji. 9 “Ga shi, kukan sa rai za ku sami da yawa, amma sai
ku ga kun sami kaɗan. Ɗan kaɗan ɗin ma da kukan kawo gida, nakan hura shi yă
tafi. Me ya sa yake faruwa haka?” In ji Ubangiji Maɗaukaki. “Saboda gidana da yake
zaman kango, yayinda kowannenku yana faman gina gidansa. 10 Shi ya sa, saboda
ku sammai sun ƙi saukar da raɓa, ƙasa kuma ta ƙi ba da amfani. 11 Na kawo fări a
ƙasar, da a kan duwatsu, da a kan hatsi, da a kan dukan abin da yake tsirowa daga
ƙasa, da a kan mutane, da a kan dabbobi da kuma a kan wahalar hannuwanku.”

12 Sa’an nan sai Zerubbabel ɗan Sheyaltiyel, da Yoshuwa ɗan Yehozadak, wanda
yake babban firist, da kuma dukan raguwar jama’ar suka yi biyayya da muryar
Ubangiji Allahnsu da kuma saƙon annabi Haggai, domin Ubangiji Allahnsu ne ya
aiko shi. Mutane kuwa suka ji tsoron Ubangiji.
13 Sai Haggai, ɗan saƙon Ubangiji, ya ba da wannan saƙo na Ubangiji ga mutane
cewa, “Ina tare da ku” in ji Ubangiji. 14 Saboda haka Ubangiji ya motsa zuciyar
Zerubbabel ɗan Sheyaltiyel, wanda yake gwamna a Yahuda, da kuma zuciyar
Yoshuwa ɗan Yehozadak, babban firist, da kuma zukatan dukan raguwar jama’ar.
Suka zo suka fara aiki a gidan Ubangiji Maɗaukaki, Allahnsu, 15 a ranar ashirin da
huɗu ga watan shida.

*Alkawarin darajar sabon gida*

A shekara ta biyu ta mulkin Sarki Dariyus,

## 2

1 a ranar ashirin da ɗaya ga watan bakwai, maganar Ubangiji ta zo ta wurin annabi
Haggai cewa, 2 “Ka yi magana da Zerubbabel ɗan Sheyaltiyel wanda yake gwamna a
Yahuda, da Yoshuwa ɗan Yehozadak, babban firist, da kuma dukan raguwar mutane.
Ka tambaye su ka ce, 3 ‘Wane ne a cikinku ya ragu da ya ga wannan gida a darajarsa
ta dā? Yaya yake a gare ku a yanzu? Bai yi kamar a bakin kome ba, ko ba haka ba?
4 Amma yanzu ka ƙarfafa, ya Zerubbabel,’ in ji Ubangiji. ‘Ka ƙarfafa, ya Yoshuwa ɗan
Yehozadak, babban firist. Ku ƙarfafa, dukanku mutanen ƙasar,’ in ji Ubangiji, ‘ku yi
aiki. Gama ina tare da ku,’ in ji Ubangiji Maɗaukaki. 5 ‘Wannan shi ne alkawarin da

na yi da ku a lokacin da kuka fito daga Masar. Ruhuna kuwa yana tare da ku. Kada
ku ji tsoro.'
6 "Ga abin da UBANGIJI Maɗaukaki ya ce, 'Ba da jimawa ba zan sāke girgiza
sammai da kuma ƙasa, teku da busasshiyar ƙasa. 7 Zan girgiza dukan al'ummai,
marmarin kowace al'umma kuma zai taso, sa'an nan zan cika gidan nan da ɗaukaka,'
in ji UBANGIJI Maɗaukaki. 8 'Da zinariya da azurfa duka nawa ne,' in ji UBANGIJI
Maɗaukaki. 9 'Daukakar gidan nan na yanzu za tă fi ɗaukakar gidan nan na dā,'
in ji UBANGIJI Maɗaukaki. 'A wannan wuri kuma zan ba da salama,' in ji UBANGIJI
Maɗaukaki."

### *Albarku saboda mutanen da suka ƙazantu*

10 A ranar ashirin da huɗu ga watan tara, a shekara ta biyu ta mulkin Dariyus,
maganar UBANGIJI ta zo wa annabi Haggai cewa, 11 "Ga abin da UBANGIJI Maɗaukaki
ya ce, 'Ku tambayi firist abin da doka ta ce. 12 Idan mutum yana riƙe da naman da aka
keɓe a rigarsa, sa'an nan kuma wannan rigar ta taɓa burodi, ko dafaffen abinci, ko
ruwan inabi, ko mai, ko kowane irin abinci, wannan zai sa abin yă zama tsarkake?' "
Firistoci suka amsa, suka ce, "A'a."
13 Sa'an nan Haggai ya ce, "In mutumin da ya ƙazantar da kansa ta wurin taɓa
gawa, ya taɓa wani daga cikin waɗannan abubuwa, za su ƙazantu?"
Firistoci suka amsa, suka ce, "I, zai ƙazantu."
14 Sai annabi Haggai ya ce, " 'Haka yake da wannan mutane da kuma wannan
al'umma a gabana,' in ji UBANGIJI. 'Duk abin da suke yi da kuma dukan abin da suke
miƙawa ƙazantattu ne.
15 " 'Yanzu kuwa sai ku yi la'akari da wannan daga wannan rana zuwa gaba*, ku
tuna yadda al'amura suke kafin a ɗora wani dutse bisa wani a haikalin UBANGIJI.
16 A lokacin, idan wani ya tafi wurin tsibin da zai auna mudu ashirin, sai yă iske
mudu goma kawai. Idan kuma wani ya tafi wurin matse ruwan inabi don yă ɗebo
lita hamsin, sai yă tarar da lita ashirin kawai. 17 Na mai da aikin da kuka sha wahala
kuka yi ya zama banza ta wurin saukar da burtuntuna, da fumfuna, da ƙanƙara,
duk da haka ba ku juyo gare ni ba,' in ji UBANGIJI. 18 'Daga wannan rana zuwa gaba,
wato, rana ta ashirin da huɗu ga watan tara, ku lura da ranar da aka kafa harsashin
haikalin UBANGIJI. Ku lura da kyau. 19 Akwai sauran irin da ya rage a rumbu? Har
yanzu, kuringar inabi da itacen ɓaure, rumman da itacen zaitun ba su ba da 'ya'ya
ba tukuna.
" 'Amma daga wannan rana zuwa gaba zan sa muku albarka.' "

### *Zerubbabel zoben kamar hatimin UBANGIJI*

20 Maganar UBANGIJI ta zo wa annabi Haggai sau na biyu a rana ta ashirin da huɗu
ga wata cewa, 21 "Ka faɗa wa Zerubbabel gwamnan Yahuda cewa zan girgiza sammai
da ƙasa. 22 Zan hamɓarar da gadajen mulki in kuma ragargaza ƙarfin ƙasashen
al'ummai. Zan tumɓuke kekunan yaƙi da mahayansu; dawakai da mahayansu za su
mutu, kowane ta wurin takobin ɗan'uwansu.
23 " 'A wannan rana,' in ji UBANGIJI Maɗaukaki, 'Zan ɗauke ka, bawana Zerubbabel
ɗan Sheyaltiyel,' in ji UBANGIJI, 'in kuma maishe ka kamar zoben hatimi, gama na
zaɓe ka,' in ji UBANGIJI Maɗaukaki."

* **2:15** Ko kuwa ranakun da suka wuce

# Zakariya

### *Kira don komawa ga Ubangiji*

1 A wata na bakwai na shekara ta biyu ta mulkin Dariyus, maganar Ubangiji ta zo
wa annabi Zakariya ɗan Berekiya ɗan Iddo.
2 "Ubangiji ya yi fushi sosai da kakanninku. 3 Saboda haka ka gaya wa mutanen,
ga abin da Ubangiji Maɗaukaki ya ce, 'Ku komo gare ni,' in ji Ubangiji Maɗaukaki,
'ni kuma zan komo gare ku,' in ji Ubangiji Maɗaukaki. 4 Kada ku zama kamar
kakanninku, waɗanda annabawa na dā suka ce musu, ga abin da Ubangiji Maɗaukaki
ya ce, 'Ku juya daga mugayen hanyoyinku da mugayen abubuwan da kuke yi.' Amma
ba su saurara ba, ko ma su kula da ni, in ji Ubangiji. 5 Yanzu ina kakanninku suke?
Annabawan kuma fa, sun rayu har abada ne? 6 Amma maganata da dokokina da na
umarta ta wurin bayina annabawa fa, ashe, ba su tabbata ba a kan kakanninku?
"Sa'an nan suka tuba suka ce, 'Ubangiji Maɗaukaki ya yi mana daidai abin da
hanyoyinmu suka cancanci mu samu, kamar dai yadda ya yi niyya yi.' "

### *Mutumin a cikin itatuwan ci-zaƙi*

7 7-8 A rana ta ashirin da huɗu ga watan goma sha ɗaya, wato, watan Shebat, a
shekara ta biyu ta Dariyus, maganar Ubangiji ta zo wa annabi Zakariya ɗan Berekiya
ɗan Iddo.
8 Da dare, na ga wahayi, a gabana kuwa ga mutum a kan jan doki! Yana tsaye
a cikin itatuwa masu furanni, a bayansa a cikin itatuwan ci-zaƙi, a bayansa kuwa
akwai dawakai masu ruwan ja, ruwan ƙasa-ƙasa da kuma ruwan fari.
9 Sai na yi tambaya na ce, "Mene ne waɗannan ranka yǎ daɗe?"
Mala'ikan da yake magana da ni ya amsa ya ce, "Zan nuna maka mene ne su."
10 Sai mutumin da yake tsaye cikin itatuwan ci-zaƙin ya yi bayani cewa, "Su ne
waɗanda Ubangiji ya aika ko'ina a duniya."
11 Sai suka ce wa mala'ikan da yake tsaye cikin itatuwan ci-zaƙin, "Mun ratsa ko'ina
a duniya, sai muka ga duniya duka tana zaman lafiya."
12 Sa'an nan mala'ikan Ubangiji ya ce, "Ya Ubangiji Maɗaukaki, har yaushe za ka
ci gaba da ƙi nuna wa Urushalima da kuma garuruwan Yahuda jinƙai, waɗanda
kake fushi da su shekarun nan saba'in?" 13 Sai Ubangiji ya yi wa mala'ikan da ya yi
magana da ni magana da kalmomi masu daɗi da kuma masu ta'azantarwa.
14 Sai mala'ikan da yake magana da ni ya ce, "Ka yi shelar maganan nan, ga abin
da Ubangiji Maɗaukaki ya ce, 'Ina kishi domin Urushalima da Sihiyona, 15 amma ina
fushi da ƙasashen da suke ji suna zaman lafiya, na ɗan yi fushina kawai, amma sai
suka ƙara musu masifar.'
16 "Saboda haka, ga abin da Ubangiji ya ce, 'Zan komo Urushalima da jinƙai, a can
ne za a sāke gina gidana. Za a kuma miƙe ma'auni a bisa Urushalima,' in ji Ubangiji
Maɗaukaki.
17 "Ci gaba da yin shela, ga abin da Ubangiji Maɗaukaki ya ce, 'Garuruwana za su
sāke kwarara da wadata, Ubangiji kuma zai sāke yi wa Sihiyona ta'aziyya, yǎ kuma
zaɓi Urushalima.' "

### *Kahoni huɗu da maƙera huɗu*

18 Sa'an nan na dubi sama a gabana kuwa sai ga ƙahoni huɗu! 19 Na tambayi
mala'ikan da yake mini magana, na ce, "Mene ne waɗannan?"
Ya amsa mini ya ce, "Waɗannan su ne ƙahonin da suka watsar da Yahuda, Isra'ila
da kuma Urushalima."

20 Sa'an nan UBANGIJI ya nuna mini maƙera guda huɗu. 21 Na yi tambaya na ce,
"Mene ne waɗannan suke zuwa yi?"
Ya amsa ya ce, "Waɗannan ne ƙahonin da suka watsar da Yahuda har ba wanda yake iya ɗaga kansa, amma maƙeran sun zo don su tsorata su su kuma saukar da ƙahonin ƙasashen nan waɗanda suka ɗaga ƙahoninsu gāba da ƙasar Yahuda don su warwatsa ta."

# 2

*Mutum riƙe da ma'auni*
1 Sa'an nan na ɗaga kai sai na ga mutum a tsaye riƙe da ma'auni a hannunsa! 2 Sai
na yi tambaya, na ce, "Ina za ka?"
Ya amsa mini ya ce, "Zan je in auna Urushalima, in ga yadda fāɗinta da tsawonta suke."
3 Sai mala'ikan da yake yi mini magana ya tafi, sai wani mala'ika ya zo ya same
shi 4 ya ce masa, "Yi gudu, gaya wa saurayin can cewa, 'Urushalima za tă zama birni
marar katanga domin mutane da dabbobi masu yawa ƙwarai za su kasance a cikinta.
5 Ni da kaina ne zan zama katangar wuta kewaye da birnin, in kuma zama darajarta,'
in ji UBANGIJI.
6 "Zo! Zo! Ku gudu daga ƙasar arewa," in ji UBANGIJI, "gama na warwatsa ku a
kusurwoyi huɗu na sama," in ji UBANGIJI.
7 "Zo, ya ke Sihiyona! Ku tsere, ku masu zama a cikin Diyar Babilon!" 8 Gama
ga abin da UBANGIJI Maɗaukaki ya ce, "Bayan ya ɗaukaka ni, ya kuma aiko ni ga
ƙasashen da suka washe ku gama duk wanda ya taɓa ku ya taɓa ƙwayar idonsa ne.
9 Ba shakka zan tā da hannuna a kansu domin bayinsu su washe su. Sa'an nan za ku
san cewa UBANGIJI Maɗaukaki ne ya aiko ni.
10 "Ki yi sowa ki yi murna, ya ke Diyar Sihiyona. Gama ina zuwa, zan zauna a
cikinki," in ji UBANGIJI. 11 "Kasashe da yawa za su haɗa kai da UBANGIJI a ranan nan,
za su kuma zama mutanena. Zan zauna a cikinku, za ku kuma san cewa UBANGIJI
Maɗaukaki ne ya aiko ni gare ku. 12 UBANGIJI zai gāji Yahuda a matsayin rabonsa a
cikin ƙasa mai tsarki zai kuma sāke zaɓi Urushalima. 13 Ku yi tsit a gaban UBANGIJI,
dukanku 'yan adam, gama ya taso daga wurin zamansa mai tsarki."

# 3

*Tufafi masu tsabta don babban firist*
1 Sa'an nan ya nuna mini Yoshuwa babban firist a tsaye a gaban mala'ikan UBANGIJI,
Shaiɗan* kuma yana tsaye a damansa don yă tuhume shi. 2 UBANGIJI ya ce wa
Shaiɗan, "UBANGIJI ya tsawata maka, Shaiɗan! UBANGIJI wanda ya zaɓi Urushalima,
ya tsawata maka! Ashe, mutumin nan ba shi ne sandar da take ƙonewa da aka ciro
daga cikin wuta ba?"
3 Yanzu an sa wa Yoshuwa tufafi masu dauda sa'ad da yake tsaye a gaban mala'ikan.
4 Mala'ikan ya ce wa waɗanda suke tsaye a gabansa, "Ku cire masa tufafinsa masu
dauda."
Sai ya ce wa Yoshuwa, "Duba, na ɗauke zunubanka, zan sa maka tufafi masu tsada."
5 Sai na ce, "Sa masa rawani mai tsabta a kansa." Aka sa masa rawani mai tsabta
a kansa aka kuma sa masa tufafi yayinda mala'ikan UBANGIJI yake tsaye a wurin.
6 Mala'ikan UBANGIJI ya yi wa Yoshuwa wannan gargaɗi. 7 "Ga abin da UBANGIJI
Maɗaukaki ya ce, 'In za ka yi tafiya a hanyoyina ka kuma kiyaye abubuwan da nake
so, za ka zama shugaban haikalina, ka kuma lura da ɗakunan shari'ata, zan kuma
ba ka wuri cikin waɗannan da suke tsaye a nan.

* **3:1** Shaiɗan yana nufin mai zargi.

8 “ ‘Ka saurara, ya babban firist Yoshuwa, kai da abokanka da suke zaune a gabanka,
ku da kuke alamun abubuwan da za su zo. Zan kawo bawana, wanda yake Reshe.
9 Dubi dutsen da na ajiye a gaban Yoshuwa! Akwai idanu bakwai† a kan wannan dutse
guda, zan kuma yi rubutu a kansa,’ in ji UBANGIJI Maɗaukaki, ‘zan kuma kawar da
zunubin ƙasan nan a rana ɗaya.
10 “ ‘A wannan rana kowannenku zai gayyaci maƙwabcinsa yă zauna a ƙarƙashin
itacen inabi da kuma na ɓaure,’ in ji UBANGIJI Maɗaukaki.”

# 4

*Wurin ajiye fitilan zinariya da itatuwan zaitun biyu*

1 Sai mala’ikan da ya yi magana da ni ya komo ya farkar da ni, kamar yadda ake
farkar da mutum daga barcinsa. 2 Ya tambaye ni ya ce, “Me ka gani?”

Na amsa, na ce, “Na ga wurin ajiye fitilan zinariya da kwano a kai, da kuma fitilu
bakwai a kansa, da butocin kai wa fitilu mai guda bakwai. 3 Akwai kuma itatuwan
zaitun guda biyu a gefensa, ɗaya a gefen dama na kwanon ɗaya kuma a gefen
hagunsa.”

4 Na tambayi mala’ikan da ya yi magana da ni na ce, “Mene ne waɗannan, ranka
yă daɗe?”

5 Sai ya amsa ya ce, “Ba ka san mene ne waɗannan ba?”

Na amsa, na ce, “A’a, ranka yă daɗe.”

6 Sai ya ce mini, “Wannan ce maganar UBANGIJI ga Zerubbabel. ‘Ba ta wurin ƙarfi
ba, ko ta wurin iko, sai dai ta wurin Ruhuna,’ in ji UBANGIJI Maɗaukaki.

7 “Kai mene ne, ya babban dutse? A gaban Zerubbabel za a rushe ka ka zama fili.
Sa’an nan Zerubbabel yă kawo dutsen da ya fi kyau, a kuma yi ta sowa ana cewa,
‘Allah yă yi masa albarka! Allah yă yi masa albarka!’ ”

8 Sai maganar UBANGIJI ta zo mini, 9 “Hannuwan Zerubbabel sun kafa harsashin
haikalin nan; hannuwansa ne kuma za su gama ginin. Sa’an nan ne za ka san cewa
UBANGIJI Maɗaukaki ne ya aiko ni zuwa wurinka.

10 “Wa ya rena ranar ƙananan abubuwa? Mutane za su yi murna sa’ad da suka ga
igiyar gwaji a hannun Zerubbabel.

“Waɗannan guda bakwai ɗin su ne idanun UBANGIJI, masu jujjuyawa cikin dukan
duniya.”

11 Sai na tambaye shi na ce, “Mene ne waɗannan itatuwan zaitun guda biyu tsaye
a hagu da kuma daman wurin ajiye fitilan fitilu?”

12 Na sāke tambaye shi na ce, “Mene ne waɗannan rassa biyun nan na zaitun a
gefen bututu biyu na zinariya da suke zuba man zinariya?”

13 Ya amsa ya ce, “Ba ka san mene ne waɗannan ba?”

Na ce, “A’a, ranka yă daɗe.”

14 Sai ya ce, “Waɗannan su ne biyun da aka shafe don* su yi wa UBANGIJI dukan
duniya hidima.”

# 5

*Naɗaɗɗen littafi mai firiya*

1 Na sāke dubawa sai ga naɗaɗɗen littafi mai firiya a gabana!

2 Sai ya tambaye ni ya ce, “Me ka gani?”

Sai na amsa na ce, “Na ga naɗaɗɗen littafi mai firiya, tsawonsa ƙafa talatin da
fāɗinsa kuma ƙafa goma sha biyar.”*

† **3:9** Ko kuwa sassa * **4:14** ko kuwa biyun da suke kawo mai su kuma * **5:2** Da Ibraniyanci tsawonsa
kamu ashirin, fāɗinsa kuma kamu goma (tsawonsa wajen mita 9, fāɗinsa kuma wajen mita huɗu da rabi).

3 Sai ya ce mini, “Wannan ce la’anar da za tă ratsa dukan ƙasar; gama bisa ga abin
da ya ce a gefe ɗaya, za a kawar da kowane ɓarawo, kuma bisa ga abin da ya ce a
ɗaya gefen za a kawar da duk mai rantsuwar ƙarya. 4 UBANGIJI Maɗaukaki ya ce,
‘Zan aika shi, zai shiga gidan ɓarawo, da gidan mai rantsuwar ƙarya da sunana. Zai
kasance a gidansa yă hallaka gidan da katakon da duwatsun.’ ”

### *Mace a cikin kwando*

5 Sai mala’ikan da yake mini magana ya zo gaba ya ce mini, “Duba ka gani ko mene
ne wannan da yake fitowa.”
6 Na tambaya na ce, “Mene ne?”
Ya amsa ya ce, “Kwando ne na awo.”† Ya ƙara da cewa, “Wannan shi ne laifin‡
mutanen a duk fāɗin ƙasar.”
7 Sa’an nan aka ɗaga murfin dalman, a ciki kuwa ga mace zaune! 8 Ya ce, “Wannan
mugunta ce,” ya kuma tura ta cikin kwandon ya rufe da murfin dalman, ya kuma
danna da dutse.
9 Na ɗaga idona sama, sai ga mata biyu a gabana, iska tana hura fikafikansu! Suna
da fikafikai kamar na shamuwa, suka kuma ɗaga kwandon sama.
10 Na tambayi mala’ikan da yake magana da ni na ce, “Ina za ku kai kwandon?”
11 Ya amsa ya ce, “Zuwa ƙasar Babiloniya§ don a gina masa haikali. Sa’ad da aka
gama ginin, za a ajiye shi a ciki.”

# 6

### *Kekunan yaƙi huɗu*

1 Na sāke ɗaga kai sama, sai ga kekunan yaƙi guda huɗu a gabana suna fitowa
tsakanin duwatsu guda biyu, duwatsun tagulla! 2 Karusa ta farko tana da jajjayen
dawakai, ta biyu kuma baƙaƙen dawakai, 3 ta ukun farare dawakai, ta huɗu kuma
dawakai masu ɗigo-ɗigo a dukan jikinsu, dukansu kuwa ƙarfafa. 4 Sai na tambayi
mala’ikan da yake magana da ni na ce, “Mene ne waɗannan, ranka yă daɗe?”
5 Mala’ikan ya amsa mini ya ce, “Waɗannan su ne ruhohi huɗu na sama, waɗanda
suka fito daga wurin Ubangiji na dukan duniya. 6 Wannan mai baƙaƙen dawakai zai
nufi wajen ƙasar arewa, mai fararen dawakai zai nufi wajen yamma, sai kuma mai
dawakai masu ɗigo-ɗigo a jiki zai nufi wajen kudu.”
7 Da ƙarfafa dawakan suka fito, sai suka yi marmari su ratsa dukan duniya. Sai ya
ce, “Ku ratsa dukan duniya!” Saboda haka suka ratsa dukan duniya.
8 Sai ya kira ni ya ce, “Duba, waɗanda suka nufi wajen ƙasar arewa sun ba wa
Ruhuna hutu a ƙasar arewa.”

### *Rawani domin Yoshuwa*

9 Maganar UBANGIJI ta zo mini, ta ce, 10 “Ka karɓi azurfa da zinariya daga masu
zaman bauta Heldai, Tobiya, Yedahiya, waɗanda suka iso daga Babilon. A ranar
kuma ka je gidan Yosiya ɗan Zefaniya. 11 Ka ɗauki azurfar da zinariyar ka yi rawani,
ka ɗora shi a kan babban firist, Yoshuwa ɗan Yehozadak. 12 Ka ce masa ga abin da
UBANGIJI Maɗaukaki ya ce, ‘Ga mutumin da sunansa ne Reshe, zai kuma ratse daga
inda yake yă gina haikalin UBANGIJI. 13 Shi ne zai gina haikalin UBANGIJI, za a kuma
martaba shi da daraja, zai kuma zauna yă yi mulki a kan kursiyinsa. Zai zama firist
a kan kursiyinsa. Kuma a tsakanin biyun za a sami zaman lafiya.’ 14 Za a ba Heldai,*
Tobiya, Yedahiya da kuma Hen† ɗan Zefaniya kamar abin tunawa a cikin haikalin

---

† **5:6** Da Ibraniyanci efa ne; haka ma a ayoyi 7-11. ‡ **5:6** ko kuwa bayyanuwar § **5:11** Da Ibraniyanci Shinar. Shinar tsohon sunan Babilon ne. Bisa ga Far 11, a wurin ne mutanen dā suka gina gini mai tsayi na saɓo ga Allah, wanda Ubangiji ya sauka ya dagula harsunansu. * **6:14** Da Siriyak da Ibraniyanci Helem † **6:14** Ko kuwa da kuma mai alheri

UBANGIJI. 15 Waɗanda suke nesa za su zo su taimaka gina haikalin UBANGIJI, za ku
kuma san cewa UBANGIJI Maɗaukaki ne ya aiko ni gare ku. Wannan zai faru in kuka
yi biyayya sosai ga UBANGIJI Allahnku."

# 7

*Gaskiya da jinƙai, ba azumi ba*

1 A shekara ta huɗu ta Sarki Dariyus, maganar UBANGIJI ta zo wa Zakariya a rana ta
huɗu ta watan tara, wato, watan Kisleb. 2 Mutanen Betel sun aika Sharezer da Regem-
Melek, tare da mutanensu su nemi tagomashin UBANGIJI 3 ta wurin tambayar firistocin
da kuma annabawan gidan UBANGIJI Maɗaukaki, "Ko ya kamata in yi makoki da
azumi a wata na biyar, yadda na yi a shekaru masu yawa?"
4 Sai maganar UBANGIJI Maɗaukaki ta zo mini ta ce, 5 "Ka tambayi dukan mutanen
ƙasar da firistoci cewa, 'Sa'ad da kuka yi makoki da azumi a wata na biyar da na
bakwai dukan shekaru saba'in nan, a ainihi saboda ni kuka yi azumi? 6 Kuma sa'ad
da kuke ci kuke sha, ba kanku kuke yi wa shagali ba? 7 Ashe, ba kalmomin da UBANGIJI
ya faɗi ke nan ta bakin annabawan farko ba sa'ad da Urushalima da garuruwan da
suke kewaye da ita suke hutawa, suke cikin wadata, akwai kuma mutane a Negeb da
yammancin gindin tuddai?' "
8 Sai maganar UBANGIJI ta sāke zuwa wa Zakariya cewa, 9 "Ga abin da UBANGIJI
Maɗaukaki ya ce, 'Ku yi shari'ar gaskiya; ku nuna jinƙai da tausayi ga juna. 10 Kada
ku danne gwauruwa ko maraya, baƙo ko talaka. A cikin zuciyarku kada ku yi mugun
tunani game da juna.'
11 "Amma suka ƙi su saurara; da taurinkai suka juya bayansu suka kuma toshe
kunnuwansu. 12 Suka taurare zukatansu kamar dutse, suka ƙi jin abin da doka ko
kuma maganar UBANGIJI Maɗaukaki take faɗi wadda ya aika ta wurin Ruhunsa ta
wurin annabawan farko. Saboda haka UBANGIJI Maɗaukaki ya ji fushi ƙwarai.
13 " 'Sa'ad da na yi kira, ba su saurara ba; saboda haka sa'ad da suka kira, ba zan
saurara ba,' in ji UBANGIJI Maɗaukaki. 14 'Na warwatsar da su da guguwa a cikin
dukan ƙasashe, inda suka zama baƙi. Aka bar ƙasar ta zama kango bayansu, da har
ba mai shiga ko fita. Haka suka sa ƙasan nan mai daɗi ta zama kango.' "

# 8

*UBANGIJI ya yi alkawari zai albarkaci Urushalima*

1 Maganar UBANGIJI Maɗaukaki ta sāke zuwa gare ni.
2 Ga abin da UBANGIJI Maɗaukaki ya ce, "Ina kishin Sihiyona ƙwarai; ina kuma cike
da kishi dominta."
3 Ga abin da UBANGIJI ya ce, "Zan koma Sihiyona in zauna a Urushalima. Sa'an nan
za a kira Urushalima Birnin Gaskiya, a kuma kira dutsen UBANGIJI Maɗaukaki Dutse
Mai Tsarki."
4 Ga abin da UBANGIJI Maɗaukaki ya ce, "Tsofaffi maza da mata za su sāke zauna
a titunan Urushalima, kowanne da sanda a hannu saboda tsufa. 5 Titunan birnin za
su cika da samari da 'yan mata suna wasa."
6 Ga abin da UBANGIJI Maɗaukaki ya ce, "Mai yiwuwa ya zama da mamaki ga
raguwar wannan mutanen da suke nan a lokacin, amma zai zama abin mamaki gare
ni ne?" In ji UBANGIJI Maɗaukaki.
7 Ga abin da UBANGIJI Maɗaukaki ya ce, "Zan ceci mutanena daga ƙasashen gabas
da yamma. 8 Zan komo da su su zauna a Urushalima; za su zama mutanena, ni kuwa
zan zama amintaccen Allahnsu mai adalci."
9 Ga abin da UBANGIJI Maɗaukaki ya ce, "Ku da yanzu kuke jin maganan nan da
annabawa suka faɗi, waɗanda suke a nan lokacin da aka kafa harsashin haikalin

UBANGIJI Maɗaukaki, bari hannuwanku su zama da ƙarfi don a gama gina haikalin.
10 Kafin wannan lokaci babu albashi domin mutum ko dabba. Ba wanda yake iya
sakewa yă yi hidimominsa saboda maƙiya, domin na sa kowa yă zama maƙiyi
maƙwabcinsa. 11 Amma yanzu ba zan yi da waɗanda raguwar mutane yadda na
yi da na dā ba," in ji UBANGIJI Maɗaukaki.
12 "Iri zai yi girma da kyau, kuringa za tă ba da 'ya'yanta, ƙasa za tă ba da hatsi,
sama kuma za tă ba da raɓa. Zan ba da duk waɗannan abubuwa su zama gādo ga
raguwar mutanen nan. 13 Kamar yadda kuka zama abin la'ana a ƙasashe, ya Yahuda
da Isra'ila, haka zan cece ku, za ku kuma zama albarka. Kada ku ji tsoro, sai dai ku
bar hannuwanku su zama da ƙarfi."
14 Ga abin da UBANGIJI Maɗaukaki ya ce, "Kamar dai yadda na yi niyyar kawo muku
bala'i, in kuma ƙi jin tausayi sa'ad da kakanninku suka ba ni haushi," in ji UBANGIJI
Maɗaukaki, 15 kada ku ji tsoro "saboda a yanzu na yi niyya in sāke yi wa Urushalima
da Yahuda abu mai kyau. 16 Abubuwan da za ku yi ke nan. Ku gaya wa juna gaskiya,
ku kuma dinga yin shari'ar gaskiya a ɗakunanku na shari'arku; 17 kada ku ƙulla
wa maƙwabtanku mugunta, kuma kada ku so yin rantsuwa ta ƙarya. Ina ƙyamar
waɗannan duka," in ji UBANGIJI Maɗaukaki.
18 Maganar UBANGIJI Maɗaukaki ta sāke zuwa wurina.
19 Ga abin da UBANGIJI Maɗaukaki ya ce, "Azumin wata na huɗu, da na watan biyar,
da na watan bakwai da na watan goma za su zama lokutan farin ciki da murna da
kuma bukukkuwa na murna ga Yahuda. Saboda haka sai ku ƙaunaci gaskiya da
salama."
20 Ga abin da UBANGIJI Maɗaukaki ya ce, "Mutane da yawa da kuma mazaunan
birane da yawa har yanzu za su zo, 21 mazaunan wani birni za su je wurin mazaunan
wani birni su ce, 'Bari mu je nan da nan mu roƙi UBANGIJI mu kuma nemi UBANGIJI
Maɗaukaki. Ni kaina zan je.' 22 Mutane da yawa kuma da al'ummai masu ƙarfi za
su zo Urushalima su nemi UBANGIJI Maɗaukaki su kuma roƙe shi."
23 Ga abin da UBANGIJI Maɗaukaki ya ce, "A kwanakin nan, mutane goma daga
kabilu da al'ummai za su riƙe rigar mutumin Yahuda guda su ce, 'Bari mu tafi tare
da kai, domin mun ji cewa Allah yana tare da ku.' "

# 9

### *Hukunci a kan abokan gāban Isra'ila*

1 Annabci.
Maganar UBANGIJI tana gāba da ƙasar Hadrak
za tă kuma sauko a kan Damaskus,
gama idanun dukan mutane da na kabilan Isra'ila
suna a kan UBANGIJI*,
2 da kuma a kan Hamat ita ma, wadda ta yi iyaka da ita,
da kuma a kan Taya da Sidon, ko da yake suna da hikima ƙwarai.
3 Taya ta gina wa kanta mafaka mai ƙarfi;
ta tara azurfa kamar ƙasa,
zinariya kuma kamar tarin shara a tituna.
4 Amma Ubangiji zai karɓe mallakarta,
zai hallaka ikonta da take da shi a kan teku,
wuta kuma za tă cinye ta.
5 Ashkelon za tă ga haka ta ji tsoro;
Gaza za tă yi birgima cikin azaba,
haka Ekron ma, gama za tă fid da zuciya.

* **9:1** Ko kuwa Damaskus. Gama idon UBANGIJI yana a kan dukan mutane, haka ma a kan kabilan Isra'ila,

Gaza za tă rasa sarkinta
za a kuma gudu a bar Ashkelon.
6 Baƙi za su mallaki Ashdod,
kuma zan kawar da girman kan Filistiyawa.
7 Zan kawar da jini daga bakinsu,
zan kuma cire abincin da aka haramta daga tsakanin haƙoransu.
Waɗanda za a bari za su zama na Allahnmu,
su kuma zama shugabanni a Yahuda,
Ekron kuma za tă zama kamar Yebusiyawa.
8 Amma zan kāre gidana
daga sojoji masu kai da kawowa.
Azzalumi ba zai ƙara cin mutanena da yaƙi ba,
gama yanzu ina tsaro.

### *Zuwan sarkin Sihiyona*

9 Ki yi murna ƙwarai, ya Diyar Urushalima!
Ki yi sowa, Diyar Urushalima!
Duba, ga sarkinki yana zuwa wurinki,
mai adalci yana kuma da ceto,
mai tawali'u yana kuma hawan jaki,
yana a kan ɗan aholaki, a kan 'yar jaka.
10 Zan ƙwace kekunan yaƙi daga Efraim,
da kuma dawakan yaƙi daga Urushalima,
za a kuma karya bakan yaƙi.
Zai yi shelar salama ga al'ummai.
Mulkinsa zai yaɗu daga teku zuwa teku,
daga Kogi† kuma zuwa ƙarshen duniya.‡
11 Ke kuma, saboda jinin alkawarina da ke,
zan 'yantar da 'yan kurkukunki daga rami marar ruwa.
12 Ku koma maɓuya, ya ku 'yan kurkuku masu sa zuciya;
ko yanzu ma na sanar cewa zan mayar muku ninki biyu.
13 Zan lanƙwasa Yahuda yadda nake lanƙwasa bakana,
in kuma cika ta da Efraim kamar kibiya.
Zan tā da 'ya'yanki maza, ya Sihiyona,
gāba da 'ya'yanki, ya Girka,
in kuma mai da ke kamar takobin jarumin yaƙi.

### *Ubangiji zai bayyana*

14 Sa'an nan Ubangiji zai bayyana a bisansu;
kibiyarsa za tă wulga kamar walƙiya.
Ubangiji Mai Iko Duka zai busa ƙaho;
zai taho ta cikin guguwa daga kudu,
15 Ubangiji Maɗaukaki kuma zai tsare su.
Za su hallakar
su kuma yi nasara da duwatsun majajjawa.
Za su sha su yi kururuwa kamar sun sha ruwan inabi;
za su cika kamar kwanon
da ake amfani don a yayyafa jini a kusurwoyin bagade.
16 Ubangiji Allahnsu zai cece su a wannan rana
gama su mutanensa ne da kuma garkensa.
Za su haska a cikin ƙasarsa

† 9:10 Wato, Yuferites ‡ 9:10 Ko kuwa ƙarshen ƙasa

kamar lu'ulu'u a rawani.
17 Za su yi kyan gani da kuma bansha'awa!
Hatsi zai sa samari su yi murna,
sabon ruwan inabi kuma zai sa 'yan mata su yi farin ciki.

# 10

*UBANGIJI zai lura da Yahuda*

1 Ku roƙi UBANGIJI yă ba ku ruwa a lokacin bazara;
UBANGIJI ne yake yin gizagizan hadari.
Shi ne yake ba wa mutane yayyafin ruwan sama
yana kuma ba da tsire-tsire na fili ga kowa.
2 Gumaka suna maganganun ruɗu,
masu duba suna ganin wahayoyin ƙarya,
suna faɗa mafarkan ƙarya
suna ba da ta'aziyyar banza.
Saboda haka mutane suna yawo kamar tumaki
waɗanda suke shan wahala saboda rashin makiyayi.

3 "Ina fushi da makiyayan,
zan kuma hukunta shugabannin;
gama UBANGIJI Maɗaukaki zai lura
da garkensa, wato, gidan Yahuda,
zai kuma sa su zama kamar doki mai fariya cikin yaƙi.
4 Daga Yahuda dutsen kusurwa zai fito,
daga gare shi za a samu abin kafa tenti,
daga gare shi za a sami bakan yaƙi,
daga gare shi za a sami kowane mai mulki.
5 Tare za su* zama kamar mutane masu ƙarfi
suna tattake lakar tituna a cikin yaƙi.
Domin UBANGIJI yana tare da su,
za su yi faɗa su kuma yi nasara a kan masu yaƙi a kan dawakai.

6 "Zan ƙarfafa gidan Yahuda
in kuma ceci gidan Yusuf.
Zan maido da su
domin ina jin tausayinsu.
Za su zama kamar
ban taɓa ƙinsu ba,
gama ni ne UBANGIJI Allahnsu
zan kuma amsa musu.
7 Mutanen Efraim za su zama kamar mutane masu ƙarfi,
zukatansu kuwa za su yi murna kamar sun sha ruwan inabi.
'Ya'yansu za su gani su yi murna;
zuciyarsu za tă yi farin ciki a cikin UBANGIJI.
8 Zan ba da alama
in kuma tattara su.
Ba shakka zan fanshe su;
za su yi yawa kamar yadda suke a dā.
9 Ko da yake na warwatsa su cikin mutane,
duk da haka a can ƙasashe masu nisa za su tuna da ni.

* **10:5** Ko kuwa mai mulki, dukansu tare. 5 Su

Su da ’ya’yansu za su rayu,
za su kuwa komo.
10 Zan komo da su daga Masar
in kuma tattara su daga Assuriya.
Zan kawo su Gileyad da Lebanon,
har wuri yă kāsa musu.
11 Za su ratsa cikin tekun wahala;
zan kwantar da raƙuman teku
dukan zurfafan Nilu kuma za su bushe.
Za a ƙasƙantar da Assuriya,
sandar sarautar Masar kuma za tă rabu da ita.
12 Zan ƙarfafa su a cikin UBANGIJI
kuma a cikin sunansa za su yi tafiya,”
in ji UBANGIJI.

# 11

1 Buɗe ƙofofinki, ya Lebanon,
don wuta ta cinye itatuwan al’ul naki.
2 Yi kuka, ya itacen fir, gama itacen al’ul ya fāɗi;
itatuwa masu daraja sun lalace!
Ku yi kuka, ku itatuwan oak na Bashan;
an sassare itatuwan babban kurmi!
3 Ku ji kukan makiyaya;
an ɓata musu wuraren kiwonsu masu ciyayi!
Ku ji rurin zakoki;
an lalatar da jejin Urdun!

*Makiyaya biyu*

4 Ga abin da UBANGIJI Allahna ya ce, “Yi kiwon garken tumakin da za a yanka.
5 Masu sayensu sun yanyanka su, suka kuwa tafi ba hukunci. Masu sayar da su sun
ce, ‘Yabi UBANGIJI, na yi arziki!’ Makiyayansu ma ba su ji tausayinsu ba. 6 Gama
ba zan ƙara jin tausayin mutanen ƙasar ba,” in ji UBANGIJI. “Zan ba da kowa ga
maƙwabcinsa da kuma sarkinsa. Za su zalunci ƙasar, ba zan kuma cece su daga
hannuwansu ba.”
7 Saboda haka na yi kiwon garken da za a yanka, musamman garken da ake zalunta.
Sai na ɗauki sanduna biyu na kira ɗaya Tagomashi, ɗaya kuma Haɗinkai, sai na yi
kiwon garken. 8 Cikin wata guda na kawar da makiyayan nan uku.

Garken suka ƙi ni, na kuwa gaji da su 9 na ce, “Ba zan zama makiyayinku ba. Bari
masu mutuwa su mutu, masu hallaka kuma su hallaka. Bari waɗanda suka ragu su
ci naman juna.”

10 Sai na ɗauki sandana mai suna Tagomashi na karya shi, na janye alkawarin da
na yi da dukan al’ummai. 11 An janye shi a ranan nan, saboda haka garken da yake
cikin wahala masu kallona sun san cewa maganar UBANGIJI ce.

12 Na faɗa musu cewa, “In kun ga ya fi kyau, ku biya ni; in kuwa ba haka ba, ku
riƙe.” Saboda haka suka biya ni azurfa talatin.

13 Sai UBANGIJI ya ce mini, “Jefar da shi cikin ma’aji,” Lada mai kyau da aka yi
cinikina ne! Saboda haka sai na ɗauki azurfa talatin ɗin na jefa su cikin gidan
UBANGIJI don a sa cikin ma’aji.

14 Sai na karya sandana na biyu mai suna Haɗinkai, ta haka na karya
’yan’uwantakar da take tsakanin Yahuda da Isra’ila.

15 Sai UBANGIJI ya ce mini, “Ka sāke ɗaukar kayan aiki na wawan makiyayi. 16 Gama
zan tā da makiyayi a ƙasar wanda ba zai kula da ɓatattu, ko yă nemi ƙanana, ko yă
warkar da waɗanda suka ji ciwo, ko kuma ciyar da masu lafiya ba, sai dai zai ci
naman keɓaɓɓun tumaki, yă farfasa kofatonsu.
17 “Kaito ga banzan makiyayin nan,
wanda ya bar garken!
Bari takobi yă sare hannunsa da idonsa na dama!
Bari hannunsa yă shanye gaba ƙaf,
idonsa na dama kuma yă makance sarai!”

# 12

*Za a hallaka abokan gāban Urushalima*
1 Annabci, maganar UBANGIJI game da Isra’ila.

UBANGIJI, wanda ya shimfiɗa sammai, wanda ya kafa harsashin duniya, wanda
kuma ya yi ruhun mutum a cikinsa ya ce, 2 “Zan sa Urushalima ta zama kwaf mai sa
mutanen da suke a dukan kewayenta, jiri. Yaƙi zai kewaye Urushalima har yă shafi
Yahuda ma. 3 A ranan nan, sa’ad da duk al’umman duniya za su tayar mata, zan sa
Urushalima ta zama dutsen da ba a iya matsarwa ga dukan al’ummai. Duk waɗanda
suka yi ƙoƙari su matsar da shi za su ji ciwo. 4 A ranan nan zan sa kowane doki
yă tsorata, mai hawan dokin kuma yă haukace,” in ji UBANGIJI. “Zan sa idanuna in
tsare gidan Yahuda, amma zan makantar da dukan dawakan al’ummai. 5 Sa’an nan
shugabannin Yahuda za su ce a cikin zukatansu, ‘Mutanen Urushalima suna da ƙarfi
domin UBANGIJI Maɗaukaki shi ne Allahnsu.’
6 “A ranan nan zan sa shugabannin Yahuda su zama kamar tukunyar wuta a tarin
itacen wuta; kamar harshen wuta a dammunan hatsi. Za su ƙone dukan mutanen da
suke kewaye da su hagu da dama, amma babu abin da zai taɓa mutanen Urushalima.
7 “UBANGIJI zai ceci wuraren zaman Yahuda da farko, don kada darajar gidan
Dawuda da mazaunan Urushalima su fi na Yahuda daraja. 8 A ranan nan UBANGIJI
zai kiyaye waɗanda suke zama a Urushalima, domin marasa ƙarfi a cikinsu su
zama kamar Dawuda, gidan Dawuda kuma zai zama kamar Allah, kamar mala’ikan
UBANGIJI da yake tafiya a gabansu. 9 A ranan nan zan fito don in hallaka dukan
al’umman da suka yaƙi Urushalima.

*Makoki saboda wannan da suka soki*
10 “Zan kuma zubo wa gidan Dawuda da mazaunan Urushalima ruhun alheri da
na addu’a. Za su dube ni, wannan da suka soke shi, za su kuma yi makoki dominsa
kamar yadda mutum yakan yi makokin mutuwar ɗansa tilo, su kuma yi baƙin ciki
ƙwarai kamar yadda mutum yakan yi baƙin ciki don ɗan fari. 11 A ranan nan kuka a
Urushalima zai yi yawa kamar kukan Hadad Rimmon a filin Megiddo. 12 Kasar za tă
yi makoki, kowane iyali zai yi makoki a ware, tare da matansu su ma a ware, iyalin
gidan Dawuda da matansu, iyalin gidan Natan da matansu, 13 iyalin gidan Lawi da
matansu, iyalin gidan Shimeyi da matansu, 14 dukan sauran iyalan kuma da matansu.

# 13

*Tsarkakewa daga zunubi*
1 “A ranan nan za a buɗe maɓulɓulan ruwa zuwa gidan Dawuda da mazaunan
Urushalima, don a tsarkake su daga zunubi da rashin tsabta.
2 “A ranan nan, zan kawar da sunayen gumaka daga ƙasar, ba kuwa za a ƙara
tunawa da su ba,” in ji UBANGIJI Maɗaukaki. “Zan kawar da annabawa da kuma

ruhu marar tsabta daga ƙasar. 3 In kuma wani ya yi annabci, sai mahaifinsa da
mahaifiyarsa su ce masa, 'Ba za ka rayu ba, gama kana faɗar ƙarya da sunan
UBANGIJI.' Sa'ad da yake yin annabci, iyayensa za su soke shi da takobi.
4 "A ranan nan kowane annabi zai ji kunyar annabcin wahayinsa. Ba zai sa rigar
annabci mai gashi ba don yă yi ruɗu. 5 Zai ce, 'Ni ba annabi ba ne. Ni manomi ne;
ƙasa ce nake samun abin zaman gari tun ina matashi.'* 6 In wani ya tambaye shi,
'Waɗanne miyaku ne haka a jikinka†?' Zai amsa yă ce, 'Miyakun da aka yi mini a
gidan abokaina ne.'

### *An bugi makiyayin, tumakin suka watse*

7 "Tashi, ya takobi, gāba da makiyayina,
mutumin da yake kusa da ni sosai!"
In ji UBANGIJI Maɗaukaki.
"Kashe makiyayin,
sai tumakin su watse,
in kuma tayar wa ƙananan.
8 A cikin ƙasar duka," in ji UBANGIJI,
"kashi biyu bisa uku za a buge su su hallaka;
duk da haka za a bar kashi ɗaya bisa uku a cikinta.
9 Wannan kashi ɗaya bisa ukun zan kawo in sa a cikin wuta;
zan tace su kamar azurfa
in gwada su kamar zinariya.
Za su kira bisa sunana
zan kuwa amsa musu;
zan ce, 'Su mutanena ne,'
za su kuma ce, 'UBANGIJI ne Allahnmu.' "

## 14

### *UBANGIJI zai zo yă yi mulki*

1 Ranar UBANGIJI tana zuwa sa'ad da za a raba muku ganimar da aka washe daga
gare ku.
2 Zan tara dukan al'ummai su yaƙi Urushalima; za a ci birnin da yaƙi, za a washe
gidaje, a kuma yi wa mata fyaɗe. Rabin birnin zai je bauta, amma ba za a kwashe
sauran mutanen daga birnin ba.
3 Sa'an nan UBANGIJI zai fita yă yi yaƙi da waɗannan al'ummai, kamar yadda yake
yaƙi a ranar yaƙi. 4 A ranan nan ƙafafunsa za su tsaya a kan Dutsen Zaitun, gabas
da Urushalima, za a kuma tsage Dutsen Zaitun kashi biyu daga gabas zuwa yamma,
yă zama babban kwari, rabin dutsen zai matsa zuwa wajen arewa, rabi kuma zai
matsa zuwa wajen kudu. 5 Za ku gudu ta wajen kwarin dutsena, gama zai miƙe har
zuwa Azel. Za ku gudu kamar yadda kuka guje wa girgizar ƙasa* a kwanakin Uzziya
sarkin Yahuda. Sa'an nan UBANGIJI Allahna zai zo, tare da duk masu tsarki.
6 A ranan nan ba za a kasance da haske ko sanyi ba, ko hazo mai duhu ba. 7 Za
tă zama rana ce ta musamman, ba yini ko dare, rana da take sananne ga UBANGIJI.
Sa'ad da yamma ta yi, za a yi haske.
8 A ranan nan ruwan rai zai kwararo daga Urushalima, rabi zai gangara gabas zuwa
teku† rabi kuma zai gangara yamma zuwa Bahar Rum,‡ a damina da rani.

* **13:5** Ko kuwa manomi; wani mutum ya sayar da a ƙuruciyata † **13:6** Ko kuwa miyaku a tsakanin hannuwanka * **14:5** Ko kuwa 5 Za a tare kwarin dutsena a kuma miƙe shi har zuwa Azel. Za a tare shi yadda aka tare saboda girgizar ƙasa † **14:8** Wato, Bahar Rum ‡ **14:8** Wato, Bahar Maliya

[9] UBANGIJI zai sama sarki bisa dukan duniya. A ranan nan za a kasance da UBANGIJI
ɗaya, ba wani suna kuma sai nasa.
[10] Kasar gaba ɗaya daga Geba zuwa Rimmon, kudu da Urushalima, za tă zama
kamar Araba. Amma Urushalima za tă kasance a wurinta, daga Kofar Benyamin
zuwa sashen Kofa ta Farko, zuwa Kofar Kusurwa, daga kuma Hasumiyar Hananel
zuwa wurin matsin ruwan inabin sarki. [11] Za a zauna a cikinka; ba za a ƙara hallaka
ta ba. Urushalima za tă zauna lafiya.
[12] Ga bala'in da UBANGIJI zai bugi dukan al'umman da suka yi yaƙi da Urushalima.
Fatar jikinsu za tă ruɓe tun suna tsaye a ƙafafunsu, idanunsu za su ruɓe a cikin
kwarminsu, harsunansu kuma zai ruɓe a cikin bakunansu. [13] A ranan nan UBANGIJI
zai sa maza su cika da tsoro ƙwarai. Kowane mutum zai kama hannun ɗan'uwansa,
za su kai wa juna hari. [14] Yahuda ma za tă yi yaƙi a Urushalima. Za a tattara dukiyar
al'umman da suke kewaye, za a tara zinariya da azurfa masu yawan gaske tare da
tufafi. [15] Irin wannan bala'i zai auko wa dawakai da alfadarai, raƙuma da jakuna,
da kuma dukan dabbobi a wannan sansani.
[16] Sa'an nan waɗanda suka tsira daga cikin al'umman da suka yaƙe Urushalima
za su haura shekara-shekara su yi wa Sarki, UBANGIJI Maɗaukaki sujada, su kuma yi
Bikin Tabanakul. [17] In waɗansu mutanen da suke duniya ba su haura Urushalima
suka yi wa Sarki, UBANGIJI Maɗaukaki sujada ba, ba za su sami ruwan sama ba.
[18] In mutanen Masar ba su haura sun yi sujada ba, ba za su sami ruwan sama ba.
UBANGIJI§ zai kawo masu bala'in da ya aika wa al'umman da ba su haura sun yi Bikin
Tabanakul ba. [19] Wannan ne zai zama hukuncin Masar da kuma na dukan al'umman
da ba su haura sun yi Bikin Tabanakul ba.
[20] A ranan nan za a rubuta TSARKI GA UBANGIJI a jikin ƙararrawar dawakai, kuma
tukwanen dahuwa a gidan UBANGIJI za su zama kamar kwanoni masu tsarki a gaban
bagade. [21] Kowace tukunya a Urushalima da Yahuda za tă zama mai tsarki ga UBANGIJI
Maɗaukaki, kuma duk wanda ya zo don miƙa hadaya zai ɗauki waɗansu tukwane
yă yi dahuwa da su. A ranan nan kuwa, ba Bakan'ane* da zai ƙara kasance a gidan
UBANGIJI Maɗaukaki.

§ **14:18** Ko kuwa sashe, sai UBANGIJI * **14:21** Ko kuwa mai ciniki

# Malaki

1 Annabci, wannan ita ce maganar UBANGIJI ga Isra’ila ta wurin Malaki.*

*An ƙaunaci Yaƙub, aka ƙi Isuwa*

2 “Na ƙaunace ku, in ji UBANGIJI.
“Amma sai kuka ce, ‘Yaya ka ƙaunace mu?’
“Isuwa ba ɗan’uwan Yaƙub ba ne?” In ji UBANGIJI. “Duk da haka na ƙaunaci
Yaƙub, 3 amma na ƙi Isuwa, na kuma mai da ƙasarsa da take kan duwatsu kango,
na ba da gādonsa ga dilolin hamada.”
4 Edom zai iya cewa, “Ko da yake an ragargaza mu, ai, za mu sāke gina kufanmu.”
Amma ga abin da UBANGIJI Maɗaukaki ya ce, “Za su iya gini, amma zan rushe. Za a
ce da su Muguwar Kasa, mutane da kullum suke a ƙarƙashi fushin UBANGIJI. 5 Za ku
ga wannan da idanunku ku kuma ce, ‘UBANGIJI da girma yake, har gaba da iyakokin
Isra’ila ma!’

*Hadayu masu aibi*

6 “Da yakan girmama mahaifinsa, bawa kuma yakan girmama maigidansa. In ni
mahaifi ne, ina girman da ya dace da ni? In ni maigida ne, ina girman da ya dace da
ni?” In ji UBANGIJI Maɗaukaki.
“Ku firistoci, ku ne kuka rena sunana.
“Amma sai kuka ce, ‘Yaya muka rena sunanka?’
7 “Kun ajiye abinci mai ƙazanta a kan bagadena.
“Sai kuka ce, ‘Yaya muka ƙazantar da kai?’
“Ta wurin cewa teburin UBANGIJI abin reni ne. 8 Sa’ad da kuka kawo makauniyar
dabba don ku miƙa mini hadaya, wannan daidai ne? Sa’ad da kuka miƙa gurguwar
dabba ko marar lafiya, wannan daidai ne? Ku gwada ba wa gwamnanku irin wannan
ku gani! Kuna gani zai ji daɗinku? Zai karɓe ku ne?” In ji UBANGIJI Maɗaukaki.
9 “To, firistoci yanzu ku gwada ku roƙi Allah yǎ yi mana alheri. Da irin hadayun
nan a hannuwanku ne zai ji ku?” In ji UBANGIJI Maɗaukaki.
10 “Kash, da ma wani daga cikinku ya rufe ƙofofin haikali don kada ku shiga, ku
hura wuta marar amfani a bisa bagadena! Ba na jin daɗinku, ba zan kuwa karɓi
hadaya daga hannuwanku ba” in ji UBANGIJI Maɗaukaki. 11 Sunana zai zama mai
girma a cikin al’ummai, daga fitowar rana har zuwa fāɗuwarta. A kowane wuri za
a miƙa wa sunana turare da tsabtacciyar hadaya domin sunana zai zama mai girma
a cikin al’ummai, in ji UBANGIJI Maɗaukaki.
12 “Amma kun ƙazantar da sunana ta wurin cewa ‘Teburin Ubangiji ya ƙazantu,’
kuka kuma yi magana a kan abincinsa kuna cewa, ‘Abin reni ne.’ 13 Kun kuma
ce, ‘Mun gaji da irin wannan wahala!’ Kuna hura mini hancin reni,” in ji UBANGIJI
Maɗaukaki.
“Sa’ad da kuka kawo raunannu, gurguntattun dabbobi, ko kuma dabbobi masu
fama da cuta, kuka kuma miƙa su hadaya, kuna gani zan karɓi wannan daga gare
ku?” In ji UBANGIJI. 14 “La’ananne ne macucin da yake da lafiyayyiyar dabba namiji a
garkensa wadda ya yi alkawari zai bayar, amma sai ya miƙa hadayar dabba mai aibi
ga Ubangiji. Gama ni babban sarki ne, za a kuma ji tsoron sunana a cikin al’ummai,”
in ji UBANGIJI Maɗaukaki.

* **1:1** Malaki yana nufin manzona.

# 2

*Karin gargaɗi ga firistoci*

1 “Yanzu fa wannan gargaɗi dominku ne, ku firistoci. 2 In ba ku saurara ba, in
kuma ba ku sa zuciyarku ga girmama sunana ba, zan aukar muku da la’ana, zan
kuma la’antar da albarkunku. I, na riga na la’anta su, domin ba ku sa zuciyarku ga
girmama ni ba, in ji Ubangiji Maɗaukaki.

3 “Saboda ku zan tsawata* wa zuriyarku;† zan watsa kashin dabbobin hadayunku a
fuskokinku, a kuma kwashe ku tare da shi. 4 Za ku kuwa san cewa ni ne na aika muku
da wannan gargaɗi domin alkawarina da Lawi yă ci gaba,” in ji Ubangiji Maɗaukaki.
5 “Alkawarina da shi, alkawari ne na rai da salama, wanda na ba shi; domin yă
girmama ni, ya kuwa girmama ni, ya kuma ji tsoron sunana ƙwarai. 6 Umarnin
gaskiya yana a bakinsa, ba a kuma sami wani ƙarya a leɓunansa ba. Ya yi tafiya tare
da ni cikin salama da adalci, ya kuwa juyo da mutane masu yawa daga zunubi.

7 “Gama ya kamata leɓunan firist su kiyaye ilimi, ya kamata kuma mutane su nemi
umarni daga bakinsa, domin shi ne manzon Ubangiji Maɗaukaki. 8 Amma sai kuka
kauce hanya, ta wurin koyarwarku kuma kuka sa mutane da yawa suka yi tuntuɓe;
kun keta alkawarin da na yi da Lawi,” in ji Ubangiji Maɗaukaki. 9 “Saboda haka na sa
a rena ku, a kuma wulaƙanta ku a gaban dukan mutane, domin ba ku bi hanyoyina
ba amma kuka nuna sonkai a al’amuran shari’a.”

*Keta alkawari ta wurin kisan aure*

10 Ashe, ba Mahaifi guda dukanmu muke da shi ba? Ba Allah ɗaya ne ya halicce
mu ba? Don me muka keta alkawarin kakanninmu ta wurin cin amanar juna?

11 Yahuda ya ci amana. An yi abin kunya a Isra’ila da kuma a Urushalima. Yahuda
ya ƙazantar da wuri mai tsarkin da Ubangiji yake ƙauna, ta wurin auren ’yar wani
baƙon allah. 12 Game da mutumin da ya aikata wannan, ko wane ne shi, bari
Ubangiji yă yanke shi daga tentunan Yaƙub,‡ ko da ma ya kawo hadayu ga Ubangiji
Maɗaukaki.

13 Ga kuma wani abin da kuke yi. Kukan cika bagaden Ubangiji da hawaye. Kukan
yi kuka kuna ihu gama Ubangiji ba ya mai da hankali ga hadayunku ko yă karɓe su
da farin ciki. 14 Kukan ce, “Don me ba ya karɓan hadayunmu?” Ai, domin Ubangiji
ya zama shaida tsakaninka da matar ƙuruciyarka, gama ka keta amanar da ka yi
mata, ko da yake ita abokiyar zamanka ce, matar aurenka ta alkawari.

15 Ashe, Ubangiji bai maishe su ɗaya ba? Cikin jiki da ruhu, su nasa ne. Me ya sa
suke ɗaya? Domin yana neman ’ya’ya masu tsoron Allah.§ Saboda haka sai ka lura
da kanka, kada kuma ka ci amanar matar ƙuruciyarka.

16 “Na ƙi kisan aure,” in ji Ubangiji, Allah na Isra’ila. “Na kuma ƙi mutumin da ya
rufe kansa da tashin hankali kamar riga,” in ji Ubangiji Maɗaukaki.

Saboda haka sai ka lura da kanka, kada kuma ka ci amana.

*Ranar shari’a*

17 Kun sa Ubangiji Maɗaukaki ya gaji da maganganunku.

Sai kuka ce, “Yaya muka sa ya gaji?”

Kun yi haka ta wurin cewa, “Duk waɗanda suke aikata mugunta, mutanen kirki ne
a gaban Ubangiji, yana kuwa jin daɗinsu,” kuna kuma cewa, “Ina Allah mai adalci
yake?”

---

* **2:3** Ko kuwa yanke (dubi Seftuwajin) † **2:3** Ko kuwa za su lalace hatsi ‡ **2:12** Ko kuwa 12 Bari Ubangiji yă yanke daga tentunan Yaƙub duk wanda ya ba da shaida a madadin mutumin da ya aikata wannan § **2:15** Ko kuwa 15 Amma wanda yake mahaifinmu bai yi haka ba, muddin yana da rai. Me yake nema? Zuriya daga Allah

# 3

[1] “Duba, zan aika manzona, wanda zai shirya hanya a gabana. Sa’an nan a farat
ɗaya Ubangiji wanda kuke nema zai zo haikalinsa. Manzon alkawari, wanda kuke
sa zuciya kuwa zai zo,” in ji Ubangiji Maɗaukaki.
[2] Amma wa zai jure wa ranar zuwansa? Wa zai iya tsaya sa’ad da ya bayyana?
Gama zai zama kamar wuta mai tace ƙarfe, ko sabulu mai wanki. [3] Zai zama kamar
mai tace azurfa da mai tsarkaketa; zai tsabtacce Lawiyawa, yǎ kuma tace su kamar
zinariya da azurfa. Sa’an nan Ubangiji zai sami mutanen da za su kawo hadayu a
cikin adalci. [4] Hadayun Yahuda da na Urushalima za su zama yardajje ga Ubangiji,
za su zama kamar a kwanakin da suka wuce, kamar a shekarun baya.
[5] “Ta haka zan zo kusa da ku don in yi hukunci. Zan hanzarta ba da shaida a kan
masu yin sihiri, da mazinata da masu shaidar zur. Zan ba da shaida a kan waɗanda
suke zaluntar ma’aikata a kan albashinsu, da waɗanda suke ƙwarar gwauraye da
marayu, suna kuma hana baƙi samun adalci, ba sa ma tsorona,” in ji Ubangiji
Maɗaukaki.

### *Keta alkawari ta wurin ƙin fid da zakka*

[6] “Ni Ubangiji ba na canjawa. Shi ya sa ku zuriyar Yaƙub, ba a hallaka ku ƙaƙaf
ba. [7] Tun zamanin kakanninku, kun juye wa ƙa’idodina baya, ba ku kuma kiyaye su
ba. Ku komo gare ni, ni kuma zan koma gare ku,” in ji Ubangiji Maɗaukaki.
“Amma sai kuka ce, ‘Yaya za mu koma gare ka?’
[8] “Mutum zai iya yi wa Allah fashi ne? Duk da haka kun yi mini fashi.
“Amma sai kuka ce, ‘Yaya muka yi maka fashi?’
“A wajen zakka da hadayu. [9] Kuna ƙarƙashin la’ana, dukan al’ummarku, domin
kuna yin mini fashi. [10] Ku kawo dukan zakka cikin gidan ajiya, don a kasance da
abinci a gidana. Ku gwada ni a wannan ku ga, ko ba zan buɗe taskokin sama in
zubo muku albarka mai yawa, wadda har ba za ku rasa wurin sa ta ba, in ji Ubangiji
Maɗaukaki. [11] Zan hana ƙwari su cinye hatsinku. Kuringar inabi a gonakinku kuma
ba za su zubar da ’ya’yansu kafin su nuna ba,” in ji Ubangiji Maɗaukaki. [12] “Sa’an
nan dukan al’ummai za su ce da ku masu albarka, gama ƙasarku za tǎ yi daɗin
zama,” in ji Ubangiji Maɗaukaki.
[13] “Kun faɗi mugayen abubuwa a kaina,” in ji Ubangiji.
“Duk da haka kuka ce, ‘Me muka faɗa a kanka?’
[14] “Kun ce, ‘Ba amfani a bauta wa Allah. Wanda amfani muka samu ta wurin
kiyaye umarnansa muna yawo kamar masu makoki a gaban Ubangiji Maɗaukaki?
[15] A ganinmu, masu girman kai suna jin daɗi. Masu aikata mugunta kuwa ba arziki
kaɗai suka yi ba, amma sukan gwada Allah da mugayen ayyukansu, su kuwa zauna
lafiya.’ ”
[16] Sa’an nan waɗanda suke tsoron Ubangiji suka yi magana da juna, Ubangiji kuwa
ya kasa kunne ya kuma ji. A gabansa aka rubuta a littafin tarihi waɗanda suke tsoron
Ubangiji, suna kuma girmama sunansa.
[17] “A ranar da na shirya ajiyayyen mallakata*, za su zama nawa,” in ji Ubangiji
Maɗaukaki. “Zan ji kansu kamar yadda mahaifi cikin tausayi yakan ji kan ɗansa
wanda yake masa hidima. [18] Za ku kuma ga bambanci tsakanin masu adalci da
mugaye, tsakanin waɗanda suke wa Allah hidima da kuma waɗanda ba sa yi.

# 4

### *Ranar Ubangiji*

* **3:17** Ko kuwa Maɗaukaki, “ajiyayyen mallakata, a ranar da na aikata”

1 “Tabbatacce rana tana zuwa; za tă yi ƙuna kamar wutar maƙera. Dukan masu
girman kai da kowane mai aikata mugunta zai zama ciyawa, wannan rana mai zuwa
za tă ƙone su. Babu saiwa ko reshen da za a bar musu,” in ji UBANGIJI Maɗaukaki.
2 Amma ku da kuke girmama sunana, ranar adalci za tă fito tare da warkarwa a
fikafikanta. Za ku kuwa fita kuna tsalle kamar ’yan maruƙan da aka sake daga garke.
3 Sa’an nan za ku tattake mugaye; za su zama toka a ƙarƙashin tafin ƙafafunku a
ranar da zan aikata waɗannan abubuwa, in ji UBANGIJI Maɗaukaki.
4 “Ku tuna da dokar bawana Musa, ƙa’idodi da dokokin da na ba shi a Horeb domin
dukan Isra’ila.
5 “Ga shi, zan aika muku da annabi Iliya kafin babbar ranan nan mai banrazana
ta UBANGIJI tă zo. 6 Zai juye zukatan iyaye ga ’ya’yansu, zukatan ’ya’ya kuma ga
iyayensu; in ba haka ba zan bugi ƙasar da hallaka gaba ɗaya.”

# Mattiyu

*Asalin Yesu Kiristi*
*(Luka 3.23-38)*

1 Tarihin da aka rubuta game da asalin Yesu Kiristi ɗan Dawuda, ɗan Ibrahim.

2 Ibrahim ya haifi Ishaku,
Ishaku ya haifi Yaƙub,
Yaƙub ya haifi Yahuda da 'yan'uwansa,
3 Yahuda ya haifi Ferez da Zera, waɗanda Tamar ce mahaifiyarsu;
Ferez ya haifi Hezron,
Hezron ya haifi Ram,
4 Ram ya haifi Amminadab,
Amminadab ya haifi Nashon,
Nashon ya haifi Salmon,
5 Salmon ya haifi Bowaz, wanda Rahab ce mahaifiyarsa,
Bowaz ya haifi Obed, wanda Rut ce mahaifiyarsa,
Obed ya haifi Yesse,
6 Yesse kuwa ya haifi Sarki Dawuda.

Dawuda ya haifi Solomon, wanda matar Uriya ce mahaifiyarsa.
7 Solomon ya haifi Rehobowam,
Rehobowam ya haifi Abiya,
Abiya ya haifi Asa,
8 Asa ya haifi Yehoshafat,
Yehoshafat ya haifi Yehoram,
Yehoram ya haifi Azariya,
9 Azariya ya haifi Yotam,
Yotam ya haifi Ahaz,
Ahaz ya haifi Hezekiya,
10 Hezekiya ya haifi Manasse,
Manasse ya haifi Amon,
Amon ya haifi Yosiya,
11 Yosiya kuma ya haifi Yekoniya* da 'yan'uwansa a lokacin da aka kwashe su zuwa bauta a Babilon.

12 Bayan an kwashe su zuwa bauta a Babilon.
Yekoniya ya haifi Sheyaltiyel,
Sheyaltiyel ya haifi Zerubbabel,
13 Zerubbabel ya haifi Abiyud,
Abiyud ya haifi Eliyakim,
Eliyakim ya haifi Azor,
14 Azor ya haifi Zadok,
Zadok ya haifi Akim,
Akim kuma ya haifi Eliyud,
15 Eliyud ya haifi Eleyazar,

* **1:11** Wato, Jehohiyachin; haka ma a aya 12

Eleyazar ya haifi Mattan,
Mattan ya haifi Yaƙub,
16 Yaƙub ya haifi Yusuf, mijin Maryamu, wadda ta haifi Yesu, wanda ake kira Kiristi.

17 Ta haka akwai zuriya goma sha huɗu ke nan duka-duka daga lokacin
Ibrahim zuwa lokacin Dawuda, goma sha huɗu kuma daga Dawuda zuwa
bauta a Babilon, goma sha huɗu kuma daga bauta a Babilon zuwa Kiristi.†

### *Haihuwar Yesu Kiristi*
### *(Luka 2.1-7)*

18 Ga yadda haihuwar Yesu Kiristi ta kasance. An yi alkawarin auren mahaifiyarsa
Maryamu, ga Yusuf. Amma tun kafin su zama miji da mata, sai aka tarar Maryamu
tana da ciki, ta wurin Ruhu Mai Tsarki. 19 Yusuf mijinta, da yake shi mai adalci ne,
bai so yă ba ta kunya, yă tone mata asiri a fili ba, sai ya yi tunani yă sake ta a ɓoye.
20 Amma yana cikin wannan tunani, sai wani mala'ikan Ubangiji ya bayyana masa
cikin mafarki ya ce, "Yusuf ɗan Dawuda, kada ka ji tsoron ɗaukan Maryamu zuwa
gidanka a matsayin matarka, gama cikin nan nata, daga wurin Ruhu Mai Tsarki ne.
21 Za tă haifi ɗa, za ka kuma sa masa suna Yesu,‡ gama shi ne zai ceci mutanensa
daga zunubansu."
22 Duk wannan ya faru ne, don a cika abin da Ubangiji ya faɗi ta bakin annabin
cewa, 23 "Ga shi budurwa za tă yi ciki, za tă haifi ɗa, kuma za a kira shi Immanuwel"§
(wanda yake nufin "Allah tare da mu").
24 Da Yusuf ya farka daga barci, sai ya bi umarnin mala'ikan Ubangiji, ya ɗauki
Maryamu zuwa gida a matsayin matarsa. 25 Amma bai kwana da ita ba, sai bayan da
ta haifi ɗan. Ya kuwa sa masa suna Yesu.

# 2

### *Ziyarar Masana*

1 Bayan an haifi Yesu a Betlehem, a Yahudiya, a zamanin Sarki Hiridus, sai waɗansu
Masana,* daga gabas suka zo Urushalima 2 suka yi tambaya suka ce, "Ina shi wanda
aka haifa sarkin Yahudawa? Gama mun ga tauraronsa a gabas† mun kuwa zo ne
domin mu yi masa sujada."
3 Da Sarki Hiridus ya ji wannan, sai hankalinsa ya tashi haka ma na dukan
Urushalima. 4 Bayan ya kira dukan manyan firistoci da malaman dokoki na mutane
wuri ɗaya, sai ya tambaye su inda za a haifi Kiristi. 5 Suka amsa suka ce, "A Betlehem
ne, cikin Yahudiya, gama haka annabin ya rubuta.
6 " 'Amma ke Betlehem, a cikin ƙasar Yahuda,
ba ke ce mafi ƙanƙanta a cikin masu mulki a Yahuda ba,
gama daga cikinki mai mulki zai zo,
wanda zai zama makiyayin mutanena Isra'ila.'‡"
7 Sai Hiridus ya kira Masanan nan a ɓoye, yă gano daga wurinsu daidai lokacin da
tauraron ya bayyana. 8 Sai ya aike su Betlehem ya ce, "Ku je ku binciko a hankali
game da yaron nan. Da kun same shi, sai ku kawo mini labari nan da nan, domin ni
ma in je in yi masa sujada."
9 Bayan sun saurari sarki, sai suka kama hanyarsu, tauraron da suka gani a gabas
kuwa yana tafe a gabansu, sai da ya kai inda yaron yake. 10 Da suka ga tauraron,
sai suka yi farin ciki ƙwarai. 11 Suka shiga gidan, suka kuwa ga yaron tare da

† **1:17** Ko kuwa Kiristi. Kiristi (Da Girik) Almasihu (Da Ibraniyanci) duk suna nufin "Shafaffe." ‡ **1:21** Yesu da Girik shi ne Yoshuwa da Ibraniyanci, wanda yake nufin UBANGIJI yana ceto. § **1:23** Ish 7.14 * **2:1** A al'adance Masu Hikima † **2:2** Ko kuwa a tauraro sa'ad da ya taso ‡ **2:6** Mik 5.2

mahaifiyarsa Maryamu. Suka durƙusa har ƙasa, suka yi masa sujada. Sa'an nan suka kunce dukiyarsu, suka miƙa masa kyautai na zinariya da na turare da na mur.
12 Bayan an gargaɗe su cikin mafarki kada su koma wurin Hiridus, sai suka koma ƙasarsu ta wata hanya dabam.

### *Tserewa zuwa Masar*

13 Bayan sun tafi, sai mala'ikan Ubangiji ya bayyana ga Yusuf a mafarki ya ce, "Tashi, ka ɗauki yaron da mahaifiyarsa, ku gudu zuwa Masar. Ku zauna a can sai na gaya muku, gama Hiridus zai nemi yaron don yǎ kashe."
14 Sai Yusuf ya tashi, ya ɗauki yaron da mahaifiyarsa da dad dare suka tafi Masar,
15 inda ya zauna har sai da Hiridus ya mutu. Ta haka kuwa aka cika abin da Ubangiji ya faɗa ta bakin annabin cewa, "Daga Masar na kira ɗana."§
16 Da Hiridus ya gane cewa Masanan nan sun yi masa wayo, sai ya husata ƙwarai, ya yi umarni cewa a karkashe dukan 'yan yara maza da suke a Betlehem da kewayenta, daga masu shekara biyu zuwa ƙasa, bisa ga lokacin da ya sami labarin daga Masanan nan. 17 Sai abin da aka faɗa ta bakin annabi Irmiya ya cika, cewa,
18 "An ji murya a Rama,
tana kuka da makoki mai tsanani,
Rahila ce take kuka domin 'ya'yanta,
an kāsa ta'azantar da ita,
don ba su."*

### *Komowa zuwa Nazaret*

19 Bayan Hiridus ya mutu, sai mala'ikan Ubangiji ya bayyana ga Yusuf a mafarki a Masar, 20 ya ce, "Tashi, ka ɗauki yaron da mahaifiyarsa ku tafi ƙasar Isra'ila, domin waɗanda suke neman ran yaron sun mutu."
21 Sai ya tashi, ya ɗauki yaron da mahaifiyarsa suka tafi ƙasar Isra'ila. 22 Amma da ya ji Arkelawus ne yake mulki a Yahudiya a matsayin wanda ya gāji mahaifinsa Hiridus, sai ya ji tsoron zuwa can. Bayan an gargaɗe shi a mafarki, sai ya ratse zuwa gundumar Galili, 23 ya je ya zauna a wani garin da ake kira Nazaret. Ta haka aka cika abin da aka faɗa ta bakin annabawa cewa, "Za a ce da shi Banazare."

# 3

### *Yohanna Mai Baftisma ya shirya hanya*
### *(Markus 1.1-8; Luka 3.1-18; Yohanna 1.19-28)*

1 A waɗancan kwanaki, Yohanna Mai Baftisma ya zo, yana wa'azi a Hamadan Yahudiya 2 yana cewa, "Ku tuba, gama mulkin sama ya yi kusa." 3 Wannan shi ne wanda aka yi maganarsa ta wurin annabi Ishaya cewa,
"Ga murya mai kira a hamada tana cewa,
'Ku shirya wa Ubangiji hanya,
ku miƙe hanyoyi dominsa.' "*
4 Tufafin Yohanna kuwa an yi su da gashin raƙumi ne, yana kuma daure da ɗamara ta fata. Abincinsa kuwa fāri ne da zumar jeji. 5 Mutane suka zo wurinsa daga Urushalima da dukan Yahudiya da kuma dukan yankin Urdun. 6 Suna furta zunubansu, ya kuma yi musu baftisma a Kogin Urdun.
7 Amma da Yohanna ya ga Farisiyawa da Sadukiyawa da yawa suna zuwa inda yake yin baftisma, sai ya ce musu, "Ku macizai! Wa ya gargaɗe ku ku guje wa fushin nan mai zuwa? 8 Ku yi ayyukan da suka dace da tuba. 9 Kada ma ku yi tunani a ranku cewa, 'Ai, Ibrahim ne mahaifinmu.' Ina gaya muku cewa Allah zai iya tā da 'ya'ya

§ **2:15** Hos 11.1 * **2:18** Irm 31.15 * **3:3** Ish 40.3

wa Ibrahim daga cikin duwatsun nan. 10 An riga an sa bakin gatari a gindin itatuwa,
kuma duk itacen da bai ba da ʼyaʼya masu kyau ba, za a sare shi a jefa cikin wuta.
11 “Ina muku baftisma da[†] ruwa domin tuba. Amma wani yana zuwa a bayana
wanda ya fi ni iko, wanda ko takalmansa ma ban isa in ɗauka ba. Zai yi muku
baftisma da Ruhu Mai Tsarki da kuma wuta. 12 Yana riƙe da matankaɗinsa, zai
tankaɗe hatsinsa, yă kuma tattara alkamarsa a cikin rumbu, amma zai ƙone yayin
da wutar da ba a iya kashewa.”

### *Baftismar Yesu*
### *(Markus 1.9-11; Luka 3.21,22)*

13 Sai Yesu ya zo daga Galili, ya je Urdun don Yohanna yă yi masa baftisma. 14 Amma
Yohanna ya so yă hana shi, yana cewa, “Ina bukata ka yi mini baftisma, yaya kake
zuwa wurina?”
15 Yesu ya amsa ya ce, “Bari yă zama haka yanzu; ya dace mu yi haka don mu cika
dukan adalci.” Saʼan nan Yohanna ya yarda.
16 Nan da nan da aka yi wa Yesu baftisma, sai ya fito daga ruwa. A wannan lokaci
sama ya buɗe, sai ya ga Ruhun Allah yana saukowa kamar kurciya ya kuwa sauka
a kansa. 17 Sai murya daga sama ta ce, “Wannan shi ne Ɗana wanda nake ƙauna;
wanda kuma nake jin daɗinsa ƙwarai.”

# 4

### *Gwajin Yesu*
### *(Markus 1.12,13; Luka 4.1-13)*

1 Saʼan nan Ruhu ya kai Yesu cikin hamada don Iblis yă gwada shi. 2 Bayan ya yi
azumi yini arbaʼin da kuma dare arbaʼin, sai ya ji yunwa. 3 Sai mai gwajin ya zo
wurinsa ya ce, “In kai Ɗan Allah ne, ka ce wa duwatsun nan su zama burodi.”
4 Yesu ya amsa ya ce, “A rubuce yake cewa, ‘Ba da abinci kaɗai mutum yake rayuwa
ba, sai dai da kowace kalmar da take fitowa daga bakin Allah.’[*]”
5 Sai Iblis ya kai shi birni mai tsarki, ya kai shi can wuri mafi tsayi duka na haikali.
6 Ya ce, “In kai Ɗan Allah ne, yi tsalle ka sauka ƙasa. Gama a rubuce yake,
“ ‘Zai umarci malaʼikunsa game da kai,
za su tallafe ka da hannuwansu,
don kada ka buga ƙafarka a kan dutse.’[†]”
7 Yesu ya amsa masa ya ce, “A rubuce yake kuma cewa, ‘Kada ka gwada Ubangiji
Allahnka.’[‡]”
8 Har wa yau, Iblis ya kai shi bisa wani dutse mai tsawo sosai, ya nunnuna masa
dukan mulkokin duniya da darajarsu. 9 Ya ce, “Zan ba ka dukan wannan, in za ka
durƙusa ka yi mini sujada.”
10 Sai Yesu ya ce masa, “Rabu da ni, Shaiɗan! Gama a rubuce yake, ‘Yi wa Ubangiji
Allahnka sujada, shi kaɗai kuma za ka bauta wa.’[§]”
11 Saʼan nan Iblis ya bar shi, malaʼiku kuwa suka zo suka yi masa hidima.

### *Yesu ya fara waʼazi*
### *(Markus 1.14,15; Luka 4.14,15)*

12 Da Yesu ya ji labari cewa an kulle Yohanna a kurkuku, sai ya koma zuwa Galili.
13 Ya bar Nazaret, ya je ya zauna a Kafarnahum, wadda take a bakin tafki wajen
Zebulun da Naftali 14 don a cika abin da aka faɗa ta bakin annabi Ishaya cewa,
15 “Kasar Zebulun da ƙasar Naftali,
da kuke a hanyar zuwa tekun Galili, a ƙetaren Urdun,
wannan yankin Galili ta Alʼummai,

---

† **3:11** Ko kuwa a cikin * **4:4** M Sh 8.3 † **4:6** Zab 91.11,12 ‡ **4:7** M Sh 6.16 § **4:10** M Sh 6.13

16 mutanen da suke zama cikin duhu
sun ga babban haske;
haske kuma ya haskaka
a kan waɗanda suke zama a inuwar mutuwa."*
17 Tun daga wannan lokaci, Yesu ya fara wa'azi yana cewa, "Ku tuba, gama mulkin
sama ya yi kusa."

*Kiran almajirai na farko*
*(Markus 1.16-20; Luka 5.1-11)*

18 Da Yesu yana kan tafiya a bakin Tekun Galili, sai ya ga waɗansu 'yan'uwa guda
biyu, Siman wanda ake kira Bitrus da ɗan'uwansa Andarawus. Suna jefa abin kamun
kifi a tafki, gama su masunta ne. 19 Sai Yesu ya ce, "Zo, ku bi ni, ni kuwa zan mai
da ku masu jan mutane zuwa wurina." 20 Nan da nan suka bar abin kamun kifinsu
suka bi shi.
21 Da ya ci gaba daga nan, sai ya ga waɗansu 'yan'uwa guda biyu, Yaƙub ɗan
Zebedi da ɗan'uwansa Yohanna. Suna cikin jirgin ruwa tare da mahaifinsu Zebedi,
suna shirya abin kamun kifinsu. Yesu ya kira su, 22 nan take suka bar jirgin ruwan
da mahaifinsu suka kuwa bi Yesu.

*Yesu ya warkar da marasa lafiya*
*(Luka 6.17-19)*

23 Yesu ya zazzaga dukan Galili, yana koyarwa a cikin majami'unsu, yana wa'azin
labari mai daɗi na mulkin sama, yana kuma warkar da kowace cuta da rashin lafiyar
mutane. 24 Labarinsa ya bazu ko'ina a Suriya, mutane kuwa suka kawo masa dukan
waɗanda suke fama da cututtuka iri-iri, da waɗanda suke da zafin ciwo, da masu
aljanu, da waɗanda suke masu farfaɗiya, da shanyayyu, ya kuwa warkar da su.
25 Taron mutane mai yawa daga Galili, Dekafolis,† Urushalima, Yahudiya da kuma
yankin hayin Urdun suka bi shi.

# 5

*Albarku*

1 Ganin taron mutane, sai ya hau kan gefen dutse ya zauna.

*(Luka 6.20-23)*

Almajiransa kuwa suka zo wurinsa, 2 sai ya fara koya musu.
Yana cewa,
3 "Masu albarka ne waɗanda suke matalauta a ruhu,
gama mulkin sama nasu ne.
4 Masu albarka ne waɗanda suke makoki,
gama za a yi musu ta'aziyya.
5 Masu albarka ne waɗanda suke masu tawali'u,
gama za su gāji duniya.
6 Masu albarka ne waɗanda suke jin yunwa da ƙishirwa don gani an yi adalci,
gama za a ƙosar da su.
7 Masu albarka ne waɗanda suke masu jinƙai,
gama za a nuna musu jinƙai.
8 Masu albarka ne waɗanda suke masu tsabtar zuciya,
gama za su ga Allah.
9 Masu albarka ne waɗanda suke masu ƙulla zumunci,
gama za a kira su 'ya'yan Allah.
10 Masu albarka ne waɗanda ake tsananta musu don gani an yi adalci,
gama mulkin sama nasu ne.

* **4:16** Ish 9.1,2f † **4:25** Wato, Birane Goma

11 “Masu albarka ne ku, sa’ad da mutane suke zaginku, suna tsananta muku, suna
kuma faɗin kowace irin muguwar magana a kanku saboda ni. 12 Ku yi murna ku
kuma yi farin ciki, domin ladarku mai yawa ne a sama, gama haka suka tsananta wa
annabawan da suka riga ku.

### *Gishiri da kuma haske*
*(Markus 9.50; Luka 14.34,35)*

13 “Ku ne gishirin duniya, amma in gishiri ya rabu da daɗin ɗanɗanonsa, yaya za
a sāke mai da daɗin ɗanɗanonsa? Ba shi da sauran amfani, sai dai a zubar da shi
mutane kuma su tattaka.
14 “Ku ne hasken duniya. Birnin da yake a bisan tudu ba ya ɓoyuwa. 15 Mutane ba
sa ƙuna fitila su rufe ta da murfi. A maimako, sukan ajiye ta a kan wurin ajiye fitila,
takan kuma ba da haske ga kowa a cikin gida. 16 Haka ma, bari haskenku yă haskaka
a gaban mutane, domin su ga ayyukanku masu kyau, su kuwa yabi Ubanku da yake
cikin sama.

### *Cikar doka*

17 “Kada ku yi tsammani na zo ne domin in kawar da Doka ko kuma Annabawa;
ban zo domin in kawar da su ba ne, sai dai domin in ciccika su. 18 Gaskiya nake gaya
muku, kafin sama da ƙasa sun shuɗe, babu ko ɗan wasali, babu wani ɗigo ta kowace
hanya da zai ɓace daga Dokar, sai an cika kome. 19 Duk wanda ya karya ɗaya daga
cikin mafi ƙanƙanta na umarnan nan, ya kuma koya wa waɗansu su yi haka, za a ce
da shi mafi ƙanƙanta a mulkin sama. Amma duk wanda ya aikata, ya kuma koyar da
waɗannan umarnai, za a kira shi mai girma a cikin mulkin sama. 20 Gama ina faɗa
muku cewa in dai adalcinku bai fi na Farisiyawa da na malaman dokoki ba, faufau,
ba za ku shiga mulkin sama ba.

### *Kisankai*

21 “Kun dai ji an faɗa wa mutanen dā cewa, ‘Kada ka yi kisankai;* kuma duk wanda
ya yi kisankai za a hukunta shi.’ 22 Amma ina gaya muku, duk wanda ya yi fushi da
ɗan’uwansa, za a hukunta shi. Kuma duk wanda ya ce wa ɗan’uwansa ‘*Raka,*’† za a
kai shi gaban Majalisa. Amma duk wanda ya ce, ‘Kai wawa!’ Zai kasance a hatsarin
shiga jahannama ta wuta.
23 “Saboda haka, in kana cikin ba da baikonka a kan bagade, a can kuwa ka tuna
cewa ɗan’uwanka yana riƙe da kai a zuci, 24 sai ka bar baikonka a can gaban bagade.
Ka je ka shirya tukuna da ɗan’uwanka; sa’an nan ka zo ka ba da baikonka.
25 “Ka yi hanzari ka shirya al’amura da maƙiyinka wanda yake ƙurarka a kotu. Ka
yi haka, tun kana tare da shi a kan hanya, in ba haka ba, zai miƙa ka ga alƙali, alƙali
kuma yă miƙa ka ga ɗan sanda, mai yiwuwa kuwa a jefa ka a kurkuku. 26 Gaskiya
nake gaya maka, ba za ka fita ba, sai ka biya kobo na ƙarshe.

### *Zina*

27 “Kun dai ji an faɗa, ‘Kada ka yi zina.’‡ 28 Amma ina gaya muku, duk wanda
ya dubi mace, sa’an nan ya yi sha’awarta a zuci, ya riga ya yi zina ke nan da ita
a zuciyarsa. 29 In idonka na dama yana sa ka yin zunubi, ƙwaƙule shi ka yar. Zai
fiye maka ka rasa ɗaya daga cikin gaɓoɓin jikinka, da a jefa jikinka ɗungum a cikin
jahannama ta wuta. 30 In kuma hannunka na dama yana sa ka yin zunubi, yanke
shi ka yar. Zai fiye maka ka rasa ɗaya daga cikin gaɓoɓin jikinka, da a jefa jikinka
ɗungum a cikin jahannama ta wuta.

### *Kashen aure*
*(Mattiyu 19.9; Markus 10.11,12; Luka 16.18)*

---

* **5:21** Fit 20.13 † **5:22** Kalmar Arameyik ta reni ‡ **5:27** Fit 20.14

31 “An kuma faɗa, ‘Duk wanda ya saki matarsa, dole yă ba ta takardar saki.’§
32 Amma ina gaya muku, duk wanda ya saki matarsa in ba a kan laifin zina ba, ya sa
ta zama mazinaciya ke nan, kuma duk wanda ya auri macen da mijinta ya sake, shi
ma yana zina ne.

### *Rantsuwa*

33 “Har wa yau dai kun ji an faɗa wa mutane a dā, ‘Kada ka karya alkawarinka,
sai dai ka cika alkawaran da ka yi wa Ubangiji.’ 34 Amma ina gaya muku, Kada ku yi
rantsuwa sam, ko da sama, domin kursiyin Allah ne; 35 ko da ƙasa, domin matashin
ƙafafunsa ne; ko kuma da Urushalima, domin birnin Babban Sarki ne. 36 Kada kuma
ka rantse da kanka, domin ba za ka iya mai da ko gashi ɗaya yă zama fari ko baƙi
ba. 37 Abin da ya kamata ku ce kawai, shi ne, I, ko A’a. Abin da ya wuce haka kuwa
daga wurin Mugun nan yake.

### *Ramuwa*
*(Luka 6.29,30)*

38 “Kun dai ji an faɗa, ‘Ido domin ido, haƙori kuma domin haƙori.’* 39 Amma ina
gaya muku, Kada ku yi tsayayya da mugun mutum. In wani ya mare ka a kumatun
dama, juya masa ɗayan ma. 40 In kuma wani yana so yă yi ƙararka yă ƙwace rigarka,
to, ba shi mayafinka ma. 41 In wani ya tilasta ka yin tafiya mil ɗaya, to, tafi tare da
shi mil biyu. 42 Ka ba wa duk wanda ya roƙe ka abu, kada kuma ka hana wa wanda
yake neman bashi daga gare ka.

### *Kauna don abokan gāba*
*(Luka 6.27,28,32-36)*

43 “Kun dai ji an faɗa, ‘Ka ƙaunaci maƙwabcinka,†ka kuma ƙi abokin gābanka.’
44 Amma ina gaya muku, ku ƙaunaci abokan gābanku‡kuma ku yi wa waɗanda suke
tsananta muku addu’a, 45 don ku zama ’ya’yan Ubanku na sama. Shi yakan sa ranarsa
ta haskaka a kan mugaye da masu kirki; yakan kuma sako ruwan sama a bisa masu
adalci da marasa adalci. 46 In masoyarku kawai kuke ƙauna, wace lada ce gare ku?
Ko masu karɓar haraji ma ba haka suke yi ba? 47 In kuwa kuna gai da ’yan’uwanku
ne kaɗai, me kuke yi fiye da waɗansu? Marasa bin Allah ma ba haka suke yi ba?
48 Saboda haka sai ku zama cikakku, yadda Ubanku na sama yake cikakke.

# 6

### *Bayarwa ga mabukata*

1 “Ku yi hankali kada ku nuna ‘ayyukanku na adalci’ a gaban mutane, don su gani.
In kuka yi haka, ba za ku sami lada daga wurin Ubanku da yake cikin sama ba.
2 “Saboda haka sa’ad da kake ba wa masu bukata taimako, kada ka yi shelarsa,
yadda munafukai suke yi a majami’u da kuma kan tituna, don mutane su yabe su.
Gaskiya nake gaya muku, sun riga sun sami ladarsu cikakke. 3 Amma sa’ad da kake ba
wa masu bukata taimako, kada ka yarda hannun hagunka yă ma san abin da hannun
damarka yake yi, 4 don bayarwarka ta zama a ɓoye. Ubanka kuwa mai ganin abin
da ake yi a ɓoye, zai sāka maka.

### *Addu’a*
*(Luka 11.2-4)*

5 “Sa’ad da kuma kuke addu’a, kada ku zama kamar munafukai, gama sun cika
son yin addu’a a tsaye a cikin majami’u da kuma a bakin titi, don mutane su gan
su. Gaskiya nake gaya muku, sun riga sun sami ladarsu cikakke. 6 Amma sa’ad da

§ **5:31** M Sh 24.1 * **5:38** Fit 21.24; Fir 24.20; M Sh 19.21 † **5:43** Fir 19.18 ‡ **5:44** Waɗansu rubuce-rubucen hannun da ba su jima ba suna da abokan gāba, ku sa wa waɗanda suke la’antarku albarka, ku yi wa waɗanda suke ƙinku alheri

kake addu’a, sai ka shiga ɗakinka, ka rufe ƙofa, ka yi addu’a ga Ubanka wanda ba a
gani. Ubanka kuwa mai ganin abin da ake yi a ɓoye, zai sāka maka. 7 Sa’ad da kuma
kuke addu’a, kada ku yi ta maimaita magana, kamar marasa sanin Allah, domin
suna tsammani za a ji su saboda yawan maganarsu. 8 Kada ku zama kamar su, gama
Ubanku ya san abin da kuke bukata kafin ma ku roƙe shi.
9 “To, ga yadda ya kamata ku yi addu’a.
“ ‘Ubanmu wanda yake cikin sama,
a tsarkake sunanka,
10 mulkinka yă zo
a aikata nufinka a duniya
kamar yadda ake yi a sama.
11 Ka ba mu yau abincin yininmu.
12 Ka gafarta mana laifofinmu,
kamar yadda mu ma muke gafarta wa masu yin mana laifi.
13 Kada ka bari a kai mu cikin jarraba,
amma ka cece mu daga mugun nan.*’
14 Gama in kuna yafe wa mutane sa’ad da suka yi muku laifi, Ubanku da yake cikin
sama ma zai gafarta muku. 15 Amma in ba kwa yafe wa mutane laifofinsu, Ubanku
ma ba zai gafarta muku zunubanku ba.

### *Azumi*

16 “Sa’ad da kuma kuna azumi, kada ku ɓata fuska, yadda munafukai suke yi.
Sukan ɓata fuskokinsu domin su nuna wa mutane cewa suna azumi. Gaskiya nake
gaya muku, sun riga sun sami ladarsu cikakke. 17 Amma sa’ad da kana azumi, ka
shafa wa kanka mai, ka wanke fuskarka, 18 domin kada mutane su ga alama cewa
kana azumi, sai dai Ubanka kaɗai wanda ba a gani; Ubanka kuwa mai ganin abin da
ake yi a ɓoye, zai sāka maka.

### *Ajiya a sama*
*(Luka 12.33,34)*

19 “Kada ku yi wa kanku ajiyar dukiya a duniya, inda asu da tsatsa suke ɓatawa,
inda kuma ɓarayi sukan fasa, su yi sata. 20 Amma ku yi wa kanku ajiyar dukiya a
sama, inda ba tsatsa da asu da za su ɓata su, inda kuma ba ɓarayin da za su fasa, su
yi sata. 21 Gama inda dukiyarka take, a nan ne fa zuciyarka za tă kasance.

*(Luka 11.34-36)*

22 “Ido shi ne fitilar jiki. In idanunka suna da kyau, dukan jikinka zai cika da
haske. 23 Amma in idanunka suna da lahani, dukan jikinka ma zai cika da duhu. To,
in hasken da yake a cikinka duhu ne, duhun ya wuce misali ke nan!

*(Luka 16.13)*

24 “Ba mai iya bauta wa iyayengiji biyu. Ko dai yă ƙi ɗaya, yă ƙaunaci ɗaya, ko
kuwa yă yi aminci ga ɗaya, sa’an nan yă rena ɗayan. Ba dama ku bauta wa Allah,
ku kuma bauta wa kuɗi gaba ɗaya.”

### *Kada ku damu*
*(Luka 12.22-31)*

25 “Saboda haka, ina gaya muku, kada ku damu game da rayuwarku, game da abin
da za ku ci, ko abin da za ku sha; ko kuma game da jikinku, game da abin da za ku
sa. Ashe, rai bai fi abinci ba, jiki kuma bai fi tufafi ba? 26 Ku dubi tsuntsayen sararin
sama mana; ba sa shuki ko girbi ko ajiya a rumbuna, duk da haka, Ubanku na sama

* **6:13** Ko kuwa daga mugu; waɗansu rubuce-rubucen hannun da ba su jima ba ɗaya, gama mulki da iko da ɗaukaka naka ne har abada. Amin.

yana ciyar da su. Ashe, ba ku fi su daraja nesa ba? 27 Wane ne a cikinku ta wurin
damuwa zai iya ƙara wa rayuwarsa ko sa'a ɗaya†?
28 "Me ya sa kuke damuwa a kan riguna? Ku dubi yadda furannin jeji suke girma
mana. Ba sa aiki ko saƙa. 29 Duk da haka ina gaya muku ko Solomon cikin dukan
darajarsa bai sa kayan adon da ya kai na ko ɗaya a cikinsu ba. 30 In haka Allah yake
yi wa ciyawar jeji sutura, wadda yau tana nan, gobe kuwa a jefa a cikin wuta, ba
zai ma fi yi muku sutura ba, ya ku masu ƙarancin bangaskiya? 31 Don haka, kada
ku damu, kuna cewa, 'Me za mu ci?' Ko, 'Me za mu sha?' Ko kuma, 'Me za mu sa?'
32 Gama marasa sanin Allah suna fama neman dukan waɗannan abubuwa, Ubanku
na sama kuwa ya san kuna bukatarsu. 33 Da farko dai, ku nemi mulkin Allah da
kuma adalcinsa, za a kuwa ba ku dukan waɗannan abubuwa. 34 Saboda haka kada
ku damu game da gobe, gama gobe zai damu da kansa. Damuwar yau ma ta isa
wahala.

## 7

*Ɗora wa waɗansu laifi*
*(Luka 6.37,38,41,42)*
1 "Kada ku ba wa kowa laifi, don kada a ba ku laifi ku ma. 2 Gama da irin shari'ar
da kuka yi wa waɗansu, da ita za a shari'anta ku. Mudun da kuka yi awo da shi, da
shi za a yi muku.
3 "Don me kake duban ɗan tsinken da yake idon ɗan'uwanka, alhali kuwa ga
gungume a naka ido? 4 Yaya za ka ce wa ɗan'uwanka, 'Bari in cire maka ɗan tsinken
nan daga idonka,' alhali kuwa a kowane lokaci akwai gungume a naka ido? 5 Kai
munafuki, fara cire gungumen da yake idonka, a sa'an nan ne za ka iya gani sosai
yadda za ka cire ɗan tsinken da yake a idon ɗan'uwanka.
6 "Kada ku ba karnuka abin da yake mai tsarki; kada kuma ku jefa wa aladu
lu'ulu'anku. In kuka yi haka za su tattake su, sa'an nan su juyo su jijji muku ciwo.

*Roƙa, nema, ƙwanƙwasa*
*(Luka 11.9-13)*
7 "Ku roƙa za a ba ku; ku nema za ku samu; ku ƙwanƙwasa za a kuwa buɗe muku
ƙofa. 8 Gama duk wanda ya roƙa, akan ba shi; wanda ya nema kuwa, yakan samu,
wanda kuma ya ƙwanƙwasa, za a buɗe masa ƙofa.
9 "Wane ne a cikinku in ɗansa ya roƙe shi burodi, sai yă ba shi dutse? 10 Ko kuwa
in ya roƙe shi kifi, sai yă ba shi maciji? 11 In ku da kuke mugaye kun san yadda za
ku ba da kyautai masu kyau ga 'ya'yanku, balle Ubanku na sama, ba zai fi ku iya ba
da abubuwa masu kyau, ga su waɗanda suka roƙe shi ba! 12 Saboda haka, duk abin
da kuke so mutane su yi muku, ku ma sai ku yi musu, domin wannan shi ne Doka da
koyarwar Annabawa sun ƙunsa.

*Matsattsiya da faɗaɗɗiyar ƙofa*
*(Luka 13.24)*
13 "Ku shiga ta matsattsiyar ƙofa. Gama ƙofar zuwa hallaka faɗaɗɗiya ce mai
sauƙin bi kuma, masu shiga ta cikinta kuwa suna da yawa. 14 Amma ƙofar zuwa rai,
ƙarama ce matsattsiya kuma, masu samunta kuwa kaɗan ne.

*Itace da 'ya'yansa*
*(Luka 6.43-45)*
15 "Ku yi hankali da annabawan ƙarya. Sukan zo muku da kamannin tumaki,
amma daga ciki mugayen kyarketai ne. 16 Ta wurin aikinsu za ku gane su. Mutane
suna iya tsinkan inabi a jikin ƙaya, ko kuwa ɓaure a jikin sarƙaƙƙiya? 17 Haka ma

† **6:27** Ko kuwa a kamu guda ga tsayinsa

kowane itace mai kyau yakan ba da ’ya’ya masu kyau, kuma mummunan itace ba ya
ba da ’ya’ya masu kyau. 18 Itace mai kyau ba ya ba da munanan ’ya’ya, haka kuma
mummunan itace ba ya ba da ’ya’ya masu kyau. 19 Duk itacen da ba ya ba da ’ya’ya
masu kyau sai a sare shi a jefa cikin wuta. 20 Ta haka, ta wurin aikinsu za ku gane
su.”

*(Luka 13.26,27)*

21 “Ba duk mai ce mini, ‘Ubangiji, Ubangiji,’ ne zai shiga mulkin sama ba, sai dai
wanda yake aikata nufin Ubana da yake sama. 22 Da yawa za su ce mini a wannan
rana, ‘Ubangiji, Ubangiji, ashe, ba mu yi annabci a cikin sunanka ba, ba kuma a
cikin sunanka ne muka fitar da aljanu, muka yi abubuwan banmamaki da yawa ba?’
23 Sa’an nan zan ce musu a fili, ‘Ban taɓa saninku ba. Ku rabu da ni, ku masu aikata
mugunta!’

### *Magini mai hikima da marar hikima*
*(Luka 6.47-49)*

24 “Saboda haka duk wanda yake jin kalmomin nan nawa yake kuma aikata su,
yana kama da mutum mai hikima wanda ya gina gidansa a kan dutse. 25 Ruwan
sama ya sauko, rafuffuka suka cika, iska kuma ta hura ta bugi gidan; duk da haka
bai fāɗi ba, gama yana da harsashinsa a kan dutse. 26 Amma duk wanda yake jin
kalmomin nan nawa bai kuwa aikata su ba, yana kama da wani wawa wanda ya
gina gidansa a kan yashi. 27 Ruwan sama ya sauko, rafuffuka suka cika, iska kuwa ta
hura ta bugi gidan, sai ya fāɗi da mummunar ragargajewa kuwa.”

28 Sa’ad da Yesu ya gama faɗin waɗannan abubuwa, sai taron mutanen suka yi
mamakin koyarwarsa, 29 domin ya koyar kamar wani wanda yake da iko, ba kamar
malamansu na dokoki ba.

# 8

### *Mutum mai kuturta*
*(Markus 1.40-45; Luka 5.12-16)*

1 Da ya sauko daga dutsen, sai taron mutane mai yawan gaske suka bi shi. 2 Wani
mutum mai kuturta ya zo ya durƙusa a gabansa ya ce, “Ubangiji, in kana so, kana
iya tsabtacce ni.”

3 Yesu ya miƙa hannunsa ya taɓa mutumin. Ya ce, “Ina so, ka tsabtacce!” Nan da
nan aka warkar[*] da shi daga kuturtarsa. 4 Sai Yesu ya ce masa, “Ka lura kada ka gaya
wa kowa. Sai dai ka tafi, ka nuna kanka ga firist ka kuma yi bayarwar da Musa ya
umarta, a matsayin shaida gare su.”

### *Bangaskiyar jarumi*
*(Luka 7.1-10; Yohanna 4.43-54)*

5 Da Yesu ya shiga Kafarnahum, sai wani jarumi ya zo wurinsa, yana neman
taimako. 6 Ya ce, “Ubangiji, bawana yana kwance a gida shanyayye, yana kuma shan
azaba ƙwarai.”

7 Yesu ya ce masa, “Zan je in warkar da shi.”

8 Jarumin ya amsa, “Ubangiji, ban cancanci in sa ka zo gidana ba, ka dai yi magana
kawai, bawana zai warke. 9 Gama ni kaina mutum ne a ƙarƙashin iko, da kuma sojoji
a ƙarƙashina. Nakan ce wa wannan, ‘Je ka,’ sai yă tafi; wancan kuma, ‘Zo nan,’ sai
yă zo. Nakan ce wa bawana, ‘Yi wannan,’ sai kuwa yă yi.”

10 Da Yesu ya ji wannan, sai ya yi mamaki ya kuma ce wa waɗanda suke binsa,
“Gaskiya nake gaya muku, ban taɓa samun wani a Isra’ila da bangaskiya mai girma
haka ba. 11 Ina kuma gaya muku da yawa za su zo daga gabas da kuma yamma,
su ɗauki wuraren zamansu a biki tare da Ibrahim, Ishaku, da Yaƙub a cikin mulkin

[*] **8:3** Girik aka tsabtacce

sama. 12 Amma za a jefar da ʼyaʼyan mulki waje, zuwa cikin baƙin duhu, inda za a
yi kuka da cizon haƙora."
13 Saʼan nan Yesu ya ce wa jarumin, "Je ka! Za a yi bisa ga bangaskiyarka." A daidai
wannan lokaci bawansa kuwa ya warke.

### *Yesu ya warkar da mutane da yawa*
*(Markus 1.29-34; Luka 4.38-41)*

14 Da Yesu ya zo cikin gidan Bitrus, sai ya ga surukar Bitrus tana kwance a gado
tana da zazzaɓi. 15 Ya taɓa hannunta sai zazzaɓin ya sake ta, ta kuwa tashi ta fara
yin masa hidima.
16 Da yamma ta yi, aka kawo masa masu aljanu da yawa, ya kuwa fitar da ruhohin
ta wurin magana, ya kuma warkar da dukan marasa lafiya. 17 Wannan ya faru ne
domin a cika abin da aka faɗa ta bakin annabi Ishaya cewa,
"Ya ɗebi rashin lafiyarmu,
ya kuma ɗauki cututtukanmu."†

### *Wahalar bin Yesu*
*(Luka 9.57-62)*

18 Da Yesu ya ga taron mutane kewaye da shi, sai ya ba da umarni a ƙetare zuwa
ɗayan hayin tafkin. 19 Sai wani malamin dokoki ya zo wurinsa ya ce, "Malam, zan bi
ka duk inda za ka."
20 Sai Yesu ya amsa ya ce, "Yanyawa suna da ramummuka, tsuntsayen sararin sama
suna da sheƙuna, amma Ɗan Mutum ba shi da wurin da zai sa kansa."
21 Sai wani almajiri ya ce masa, "Ubangiji, da farko bari in je in binne mahaifina."
22 Amma Yesu ya ce masa, "Ka bi ni, ka bar matattu su binne matattunsu."

### *Yesu ya kwantar da hadari*
*(Markus 4.35-41; Luka 8.22-25)*

23 Sai ya shiga jirgin ruwa, almajiransa kuwa suka bi shi. 24 Ba zato ba tsammani,
sai wani babban hadari ya taso a tafkin, har raƙuman ruwan suka sha kan jirgin.
Amma Yesu yana barci. 25 Almajiran suka je suka tashe shi, suna cewa, "Ubangiji, ka
cece mu! Za mu nutse!"
26 Ya amsa ya ce, "Ku masu ƙarancin bangaskiya, me ya sa kuke tsoro haka?" Saʼan
nan ya tashi ya tsawata wa iskar da kuma raƙuman ruwan, sai wuri ya yi tsit gaba
ɗaya.
27 Mutanen suka yi mamaki suka ce, "Wane irin mutum ne wannan? Har iska da
raƙuman ruwa suna masa biyayya!"

### *Warkar da mutum biyu masu aljanu*
*(Markus 5.1-20; Luka 8.26-39)*

28 Da ya isa ɗayan gefen a yankin Gadarenawa‡ (ko kuwa Gerasenawa), sai ga
mutum biyu masu aljanu suna fitowa daga kaburbura suka tarye shi. Su abin tsoro
ne ƙwarai, har ba mai iya bin wannan hanya. 29 Suka yi ihu suka ce, "Me ya haɗa
ka da mu, Ɗan Allah?" Ka zo ne nan don ka ji mana kafin lokaci yǎ yi?
30 Nesa kaɗan da su kuwa akwai babban garken aladu da yake kiwo. 31 Aljanun
suka roƙi Yesu suka ce, "In ka fitar da mu, tura mu cikin garken aladun nan."
32 Ya ce musu, "Ku tafi!" Sai suka fita suka shiga cikin aladun, dukan garken kuwa
ya gangara a guje daga kan tudun zuwa cikin tafkin aladun kuma suka mutu a cikin
ruwa. 33 Masu kiwon aladun suka ruga, suka je cikin gari suka ba da labarin dukan
wannan, haɗe da abin da ya faru da mutanen nan masu aljanu. 34 Sai dukan garin

† **8:17** Ish 53.4 ‡ **8:28** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da Gergesenawa; waɗansu kuma Gerasenawa ne a nan

suka fito don su taryi Yesu. Da suka kuwa gan shi, sai suka roƙe shi yǎ bar musu
yanki.

# 9

### *Yesu ya warkar da shanyayye*
### *(Markus 2.1-12; Luka 5.17-26)*

1 Yesu ya shiga jirgin ruwa, ya ƙetare ya zo garinsa. 2 Waɗansu mutane suka kawo
masa wani shanyayye, kwance a tabarma. Da Yesu ya ga bangaskiyarsu, sai ya ce wa
shanyayyen, “Kada ka damu saurayi, an gafarta maka zunubanka.”
3 Da jin wannan, waɗansu malaman dokoki suka ce wa juna, “Wannan mutum
yana yin saɓo!”
4 Sane da tunaninsu, Yesu ya ce, “Me ya sa kuke da mugun tunani a zuciyarku?
5 Wanne ya fi sauƙi, a ce, ‘An gafarta maka zunubanka,’ ko kuwa a ce, ‘Tashi
ka yi tafiya?’ 6 Amma don ku san cewa Ɗan Mutum yana da iko a duniya yǎ
gafarta zunubai.” Sai ya ce wa shanyayyen, “Tashi, ɗauki tabarmarka ka tafi gida.”
7 Mutumin kuwa ya tashi ya tafi gida. 8 Da taron suka ga haka, sai suka cika da tsoro,
suka yabi Allah wanda ya ba wa mutane irin ikon nan.

### *Kiran Mattiyu*
### *(Markus 2.13-17; Luka 5.27-32)*

9 Da Yesu ya yi gaba daga wurin, sai ya ga wani mutum mai suna Mattiyu zaune a
inda ake karɓar haraji. Ya ce masa, “Bi ni.” Mattiyu kuwa ya tashi ya bi shi.
10 Yayinda Yesu yake cin abinci a gidan Mattiyu, masu karɓar haraji da yawa da
kuma masu zunubi suka zo suka kuwa ci tare da shi da kuma almajiransa. 11 Saʼad da
Farisiyawa suka ga haka, sai suka tambayi almajiransa suka ce, “Don me malaminku
yake ci tare da masu karɓar haraji, da masu zunubi?”
12 Da jin wannan, Yesu ya ce, “Ai, ba masu lafiya ba ne su bukatar likita, sai dai
marasa lafiya. 13 Amma ku je ku koyi abin da wannan yake nufi, ‘Jinƙai nake bukata,
ba hadaya ba.’*Gama ban zo domin in kira masu adalci ba, sai dai masu zunubi.”

### *An Tuhumi Yesu game da azumi*
### *(Markus 2.18-22; Luka 5.33-39)*

14 Sai almajiran Yohanna suka zo suka tambaye shi suka ce, “Me ya sa mu da
Farisiyawa muke azumi, amma almajiranka ba sa yi?”
15 Yesu ya amsa ya ce, “Yaya baƙin ango za su yi makoki yayinda yake tare da su?
Lokaci yana zuwa da za a ɗauke ango daga gare su, saʼan nan za su yi azumi.
16 “Ba mai yin faci da sabon ƙyalle a kan tsohuwar riga, gama facin zai kece rigar
yǎ sa kecewar ma ta fi ta dā muni. 17 Mutane kuma ba sa zuba sabon ruwan inabi a
cikin tsofaffin salkuna. In suka yi haka, salkunan za su farfashe, ruwan inabin kuwa
yǎ zube salkunan kuma su lalace. Aʼa, ai, sukan zuba sabon ruwan inabi ne a cikin
sababbin salkuna, don a kiyaye dukan biyun.”

### *Yarinya da ta mutu da kuma mace marar lafiya*
### *(Markus 5.21-43; Luka 8.40-56)*

18 Yayinda yake faɗin wannan, sai wani mai mulki ya zo ya durƙusa a gabansa
ya ce, “Yanzu-yanzu diyata ta rasu. Amma ka zo ka ɗibiya hannunka a kanta, za tǎ
kuwa rayu.” 19 Yesu ya tashi ya tafi tare da shi, haka ma almajiransa.
20 A daidai wannan lokaci sai ga wata mace wadda ta yi shekaru goma sha biyu
tana zub da jini ta raɓo ta bayansa ta taɓa gefen rigarsa. 21 Ta ce a ranta, “Ko da
rigarsa ce kawai na taɓo, zan warke.”

* **9:13** Hos 6.6

22 Yesu ya juya ya gan ta. Sai ya ce, “Kada ki damu diyata, bangaskiyarki ta warkar
da ke.” Nan take macen ta warke.
23 Da Yesu ya shiga gidan mai mulkin ya ga masu busan sarewa da taro mai
hayaniya, 24 sai ya ce, “Ku ba da wuri. Ai, yarinyar ba tă mutu ba, tana barci ne.”
Amma suka yi masa dariya. 25 Bayan an fitar da taron waje, sai ya shiga ciki ya kama
yarinyar a hannu, ta kuwa tashi. 26 Labarin wannan kuwa ya bazu koʼina a yankin.

*Yesu ya warkar da makafi da kuma kurame*

27 Da Yesu ya fita daga can, sai waɗansu makafi biyu suka bi shi, suna kira, suna
cewa, “Ka yi mana jinƙai, Ɗan Dawuda!”
28 Da ya shiga cikin gida, sai makafin nan suka zo wurinsa, ya kuma tambaye su,
“Kun gaskata cewa ina iya yin wannan?”
Suka amsa suka ce, “I, Ubangiji.”
29 Saʼan nan ya taɓa idanunsu ya ce, “Bisa ga bangaskiyarku a yi muku haka”; 30 sai
idanunsu suka buɗe. Yesu ya gargaɗe su sosai ya ce, “Ku lura kada wani yă san wani
abu game da wannan.” 31 Amma suka fita suka yi ta baza labari game da shi koʼina
a wannan yankin.
32 Yayinda suke fitowa, sai aka kawo wa Yesu wani mutum mai aljani, da ba ya iya
magana. 33 Saʼad da aka fitar da aljanin kuwa, sai beben ya yi magana. Taron suka
yi mamaki suka ce, “Ba a taɓa ganin irin wannan abu a Israʼila ba.”
34 Amma Farisiyawa suka ce, “Ai, da ikon sarkin aljanu yake fitar da aljanu.”

*Maʼaikata kaɗan ne*

35 Yesu ya zazzaga dukan garuruwa da ƙauyuka, yana koyarwa a majamiʼunsu,
yana waʼazin labari mai daɗi na mulkin yana kuma warkar da kowace irin cuta da
rashin lafiya. 36 Da ya ga taron mutane, sai ya ji tausayinsu, domin an wulaƙanta
su ba su kuma da mai taimako, kamar tumaki marasa makiyayi. 37 Sai ya ce wa
almajiransa, “Girbi yana da yawa, amma maʼaikata kaɗan ne. 38 Saboda haka ku
roƙi Ubangijin girbi, yă aiko da maʼaikata cikin gonarsa na girbi.”

## 10

*Yesu ya aiki sha biyun*
*(Markus 3.13-19; Luka 6.12-16)*

1 Sai ya kira almajiransa goma sha biyu wurinsa ya kuma ba su iko su fitar aljanu,
su kuma warkar da kowace irin cuta da rashin lafiya.

2 Ga sunayen manzannin nan goma sha biyu,

da fari, Siman (wanda ake kira Bitrus) da ɗanʼuwansa Andarawus;
Yaƙub ɗan Zebedi da ɗanʼuwansa Yohanna;
3 Filibus da Bartolomeyu;
Toma da Mattiyu mai karɓar haraji;
Yaƙub ɗan Alfayus da Taddayus;
4 Siman Zilot da kuma Yahuda Iskariyot wanda ya bashe Yesu.

*(Markus 3.13-19; Luka 6.12-16)*

5 Waɗannan sha biyun ne Yesu ya aika da umarni cewa, “Kada ku je cikin Alʼummai,
ko kuwa ku shiga wani garin Samariyawa. 6 A maimakon haka ku je wajen ɓatattun
tumakin Israʼila. 7 Saʼad da kuke tafiya, ku yi waʼazi, kuna cewa, ‘Mulkin sama ya
kusato.’ 8 Ku warkar da marasa lafiya, ku tā da matattu, ku tsabtacce kutare, ku kuma
fitar da aljanu. A kyauta kuka samu, ku kuma bayar a kyauta.

9 “Kada ku riƙe wata zinariya ko azurfa ko jan ƙarfe a aljihunanku, 10 kada ku ɗauki
jaka don tafiya, ko ƙarin riga, ko takalma ko sanda; domin ma’aikaci ya cancanci
hakkinsa. 11 Kowane gari ko ƙauyen da kuka shiga, ku nemi mai mutunci a wurin,
ku kuma zauna a gidansa har sai kun tashi. 12 Da shigarku gidan, ku yi gaisuwa.
13 In gidan na kirki ne, bari salamarku ta zauna a kansa; in kuwa ba mai kirki
ba, salamarku ta komo muku. 14 Duk wanda ya ƙi marabtarku ko ya ƙi sauraron
kalmominku, sai ku karkaɗe ƙurar ƙafafunku sa’ad da kuka fita gidan ko garin.
15 Gaskiya nake gaya muku, za a fi jin tausayin Sodom da Gomorra a ranar shari’a
fiye da wannan gari.

*(Markus 3.13-19; Luka 6.12-16)*

16 “Ina aikan ku kamar tumaki a cikin kyarketai. Saboda haka ku zama masu wayo
kamar macizai, kuma marasa ɓarna kamar kurciyoyi. 17 Ku yi hankali da mutane; za
su miƙa ku ga majalisa su kuma yi muku bulala a majami’unsu. 18 Saboda ni, za a ja
ku zuwa gaban gwamnoni da gaban sarakuna domin ku ba da shaida a gabansu, da
kuma ga Al’ummai. 19 Amma sa’ad da suka kama ku, kada ku damu game da abin
da za ku faɗa ko kuwa yadda za ku faɗe shi. A lokacin za a ba ku abin da za ku
faɗa, 20 gama ba ku ba ne kuke magana, amma Ruhun Ubanku ne yake magana ta
wurinku.
21 “Ɗan’uwa zai ci amanar ɗan’uwansa, a kuma kashe shi, Uba ma zai yi haka da
ɗansa; ’ya’ya za su tayar wa iyayensu, su kuma sa a kashe su. 22 Dukan mutane za
su ƙi ku saboda ni, amma wanda ya jure har ƙarshe zai sami ceto. 23 Sa’ad da aka
tsananta muku a wannan wuri, ku gudu zuwa wancan. Gaskiya nake gaya muku,
kafin ku gama zazzaga dukan biranen Isra’ila, Ɗan Mutum zai zo.
24 “Dalibi ba ya fin malaminsa, haka ma, bawa ba ya fin maigidansa. 25 Ya isa wa
ɗalibi yă zama kamar malaminsa, haka ma bawa kamar maigidansa. In har an kira
wanda yake kan gida Be’elzebub,* me za su ce game da mutanen gidansa?

*(Luka 12.2-7)*

26 “Saboda haka kada ku ji tsoronsu. Ba abin da yake a rufe da ba za a tone ba, ko
kuwa a ɓoye da ba za a bayyana ba. 27 Abin da na faɗa muku a asirce, ku faɗe shi a
sarari; abin da aka faɗa muku a kunne, ku yi shelarsa daga kan rufin ɗaki. 28 Kada
ku ji tsoron masu kashe jiki amma ba sa iya kashe rai. A maimakon haka, ku ji tsoron
Wannan wanda yake da iko yă hallaka rai duk da jiki a jahannama ta wuta. 29 Ba
akan sayar da kanari biyu kobo ɗaya ba? Duk da haka ba ɗayansu da zai fāɗi ƙasa
ba da yardar Ubanku. 30 Kai, ko gashin kanku ma duk an ƙidaya su. 31 Saboda haka
kada ku ji tsoro; kun fi kanari masu yawa, daraja nesa.

*(Luka 12.8,9)*

32 “Duk wanda ya bayyana yarda a gare ni a gaban mutane, ni ma zan bayyana
yarda a gare shi a gaban Ubana da yake cikin sama. 33 Amma duk wanda ya yi mūsun
sani na a gaban mutane, ni ma zan yi mūsun saninsa a gaban Ubana da yake cikin
sama.

*(Luka 12.51-53; 14.26,27)*

34 “Kada fa ku ɗauka na zo ne don in kawo salama a duniya. A’a, ban zo don in
kawo salama ba, sai dai takobi. 35 Gama na zo ne in sa,
“ ‘gāba tsakanin mutum da mahaifinsa,
’ya da mahaifiyarta,
matar ɗa da surukarta,
36 abokan gāban mutum, za su zama mutanen gidansa ne.’†
37 “Duk wanda ya fi ƙaunar mahaifinsa ko mahaifiyarsa fiye da ni, bai dace yă
zama nawa ba; duk kuwa wanda yake ƙaunar ɗansa ko diyarsa fiye da ni, bai dace

* **10:25** Da Girik Be’ezebowul ko kuwa Be’elzebowul † **10:36** Mik 7.6

yă zama nawa ba; [38] duk wanda kuma bai ɗauki gicciyensa ya bi ni ba, bai dace yă
zama nawa ba. [39] Duk mai son adana ransa zai rasa shi, duk wanda kuwa ya rasa
ransa saboda ni zai same shi.

*(Markus 9.41)*

[40] "Wanda ya karɓe ku, ya karɓe ni ne, wanda kuma ya karɓe ni, ya karɓi wanda
ya aiko ni ne. [41] Duk wanda ya karɓi annabi don shi annabi ne, zai sami ladar annabi,
duk kuwa wanda ya karɓi mutum mai adalci don shi mai adalci ne, zai sami ladar
mai adalci. [42] In kuma wani ya ba wa ɗaya daga cikin ƙananan nan ko da kwaf
ruwan sanyi ne kan shi almajirina ne, gaskiya nake gaya muku, ba shakka ba zai
rasa ladarsa ba."

# 11

*Yesu da Yohanna Mai Baftisma*

*(Luka 7.18-35)*

[1] Bayan Yesu ya gama yi wa almajiransa sha biyun nan umarni, sai ya yi gaba daga
can don yă koyar yă kuma yi wa'azi a garuruwan Galili.*

[2] Sa'ad da Yohanna Mai Baftisma ya ji a kurkuku abin da Kiristi yake yi, sai ya aiki
almajiransa [3] su tambaye shi, "Kai ne wanda zai zo, ko kuwa mu sa ido ga wani?"

[4] Yesu ya amsa ya ce, "Ku koma ku gaya wa Yohanna abin da kuka ji, kuka kuma
gani. [5] Makafi suna gani, guragu suna tafiya, ana warkar da waɗanda suke da kuturta,
kurame suna ji, ana tā da matattu, ana kuma yi wa matalauta wa'azin labari mai daɗi.
[6] Mai albarka ne mutumin da bai yi tuntuɓe ba saboda ni."

[7] Sa'ad da almajiran Yohanna suke barin wurin, sai Yesu ya fara yi wa taron magana
game da Yohanna. "Me kuka je kallo a hamada? Ciyawar da iska take kaɗawa ne?
[8] In ba haka ba, to, me kuka je kallo? Mutum mai sanye da riguna masu kyau ne?
A'a, masu sa riguna masu kyau, ai, a fadan sarakuna suke. [9] To, me kuka je kallo
ne? Annabi? I, ina gaya muku, ya ma fi annabi. [10] Wannan shi ne wanda aka rubuta
game da shi cewa,

" 'Zan aiki ɗan saƙona yă sha gabanka,
wanda zai shirya hanyarka a gabanka.'†

[11] Gaskiya nake gaya muku. A cikin dukan waɗanda mata suka haifa, ba wani da
ya taso da ya fi Yohanna Mai Baftisma girma; duk da haka mafi ƙanƙanta a mulkin
sama ya fi shi girma. [12] Tun daga kwanakin Yohanna Mai Baftisma har yă zuwa
yanzu, mulkin sama yana sha da ƙyar, fitanannu kuma sun kama mulkin sama sun
riƙe gam. [13] Gama dukan Annabawa da kuma Doka sun yi ta annabci har yă zuwa
kan Yohanna. [14] In kuna niyya ku yarda da wannan, to, shi ne Iliya da dā ma zai zo.
[15] Duk mai kunnen ji, yă ji.

[16] "Da me zan kwatanta wannan zamani? Suna kama da yara da suke zaune a
kasuwa, suna kiran juna, suna cewa,

[17] " 'Mun yi muku busa,
ba ku kuwa yi rawa ba,
mun rera waƙar makoki,
ba ku kuwa yi makoki ba.'

[18] Gama Yohanna Mai Baftisma ya zo ba ya ciye-ciye, ba ya shaye-shaye, sai suka ce,
'Ai, yana da aljani.' [19] Ɗan Mutum ya zo yana ciye-ciye, yana shaye-shaye, sai suka
ce, 'Ga mai haɗama da kuma mashayi, abokin masu karɓar haraji da masu zunubi.'
Amma akan tabbatar da hikima ta wurin ayyukanta."

* **11:1** Da Girik a cikin garuruwansu † **11:10** Mal 3.1

*Kaiton biranen da ba su tuba ba*
*(Luka 7.18-35)*

20 Sai Yesu ya fara yin tir da biranen da aka yi yawancin ayyukansa na banmamaki,
don ba su tuba ba. 21 “Kaitonki, Korazin! Kaitonki, Betsaida! Da a ce ayyukan
banmamakin da aka yi a cikinki ne aka yi a Taya da Sidon, da tuni sun tuba sanye
da rigar makoki da toka. 22 Amma ina gaya muku, za a fi jin tausayin Taya da Sidon
a ranar shari’a, fiye da ku. 23 Ke kuma Kafarnahum, za a ɗaga ki sama ne? A’a, za ki
gangara zuwa zurfafa ne. Da a ce ayyukan banmamakin da aka yi a cikinki ne a aka
yi a Sodom, da tana nan har yǎ zuwa yau. 24 Amma ina gaya miki, za a fi jin tausayin
Sodom fiye da ke a ranar shari’a.”

*Hutu domin waɗanda suka gaji*
*(Luka 10.13-15)*

25 A wannan lokaci sai Yesu ya ce, “Ina yabonka, Uba, Ubangijin sama da ƙasa,
gama ka ɓoye waɗannan abubuwa ga masu hikima da masu ilimi, ka kuma bayyana
su ga ƙananan yara. 26 I, Uba, gama wannan shi ne abin da ka ji daɗin yi.
27 “Dukan kome Ubana ya danƙa mini. Ba wanda ya san Ɗan sai dai Uban, ba kuma
wanda ya san Uban, sai dai Ɗan da kuma waɗanda Ɗan ya so yǎ bayyana musu shi.
28 “Ku zo gare ni, dukanku da kuka gaji kuke kuma fama da kaya, zan kuwa ba ku
hutu. 29 Ku ɗauki karkiyata a kanku, ku kuma yi koyi da ni, gama ni mai tawali’u
ne marar girman kai, za ku kuwa sami hutu don rayukanku. 30 Gama karkiyata mai
sauƙi ce, kayana kuma marasa nauyi ne.”

# 12

*Ubangijin Asabbaci*
*(Markus 2.23-28; Luka 6.1-5)*

1 A lokacin nan Yesu ya bi ta gonakin hatsi a ranar Asabbaci. Almajiransa kuwa
suna jin yunwa, sai suka fara kakkarya kan hatsi suna ci. 2 Sa’ad da Farisiyawa suka
ga wannan, sai suka ce masa, “Duba! Almajiranka suna yin abin da doka ta hana a
yi a ranar Asabbaci.”
3 Sai ya amsa ya ce, “Ba ku karanta abin da Dawuda ya yi ba ne sa’ad da shi da
abokan tafiyarsa suka ji yunwa? 4 Ya shiga gidan Allah, da shi da abokan tafiyarsa
suka ci keɓaɓɓen burodin, wanda doka ta hana su yi, sai firistoci kaɗai. 5 Ko kuwa ba
ku karanta a Doka cewa a ranar Asabbaci firistoci sukan karya dokar Asabbaci duk
da haka ba da yin wani laifi ba? 6 Ina faɗa muku cewa wani*wanda ya fi haikali yana
a nan. 7 Da a ce kun san abin da waɗannan kalmomi suke nufi, ‘Jinƙai nake bukata,
ba hadaya ba,’†da ba ku zargi marar laifi ba. 8 Gama Ɗan Mutum shi ne Ubangijin
Asabbaci.”

*(Markus 3.1-6; Luka 6.6-11)*

9 Da ya ci gaba daga wurin, sai ya shiga majami’arsu, 10 a nan kuwa akwai wani
mutum mai shanyayyen hannu. Don neman dalili su zargi Yesu, sai suka tambaye
shi suka ce, “Ya dace a warkar a ranar Asabbaci?”
11 Ya ce musu, “In waninku yana da tunkiya, ta kuma fāɗa a rami ran Asabbaci, ba
zai cire ta daga ramin ba? 12 Sau nawa mutum ya fi tunkiya daraja! Saboda haka ya
dace a aikata alheri ran Asabbaci.”
13 Sa’an nan ya ce wa mutumin, “Miƙa hannunka.” Sai ya miƙa, hannunsa kuwa ya
koma lafiyayye, kamar dai ɗayan. 14 Amma Farisiyawa suka fita suka ƙulla shawara
yadda za su kashe Yesu.

*Zaɓaɓɓen bawan Allah*

* **12:6** Ko kuwa a wani abu; haka ma a ayoyi 41 da 42 † **12:7** Hos 6.6

15 Da ya gane wannan, sai Yesu ya janye daga wurin. Da yawa suka bi shi, ya
kuwa warkar da dukan masu ciwonsu, 16 yana jan musu kunne kada su faɗa wa
kowa akan ko shi wane ne. 17 Wannan kuwa domin a cika abin da aka faɗa ta bakin
annabi Ishaya ne cewa,
18 “Ga bawana da na zaɓa,
ƙaunataccena, wanda nake farin ciki da shi;
zan sa Ruhuna a kansa,
zai kuma yi shelar adalci ga al’ummai.
19 Ba zai yi faɗa ko yǎ ɗaga murya ba,
ba kuwa wanda zai ji muryarsa a kan tituna.
20 Kyauron da ya tanƙwasa ba zai karye shi ba.
Fitilar da ta yi kusan mutuwa ba zai kashe ta ba,
sai ya jagoranci adalci zuwa ga nasara.
21 Cikin sunansa al’ummai za su dogara.”‡

*Yesu da Be’elzebub*
*(Markus 3.20-30; Luka 11.14-23; 12.10)*

22 Sai aka kawo masa wani bebe kuma makaho mai aljani, Yesu kuwa ya warkar da
shi, har ya iya magana ya kuma sami ganin gari. 23 Dukan mutane suka yi mamaki,
suka ce, “Wannan Ɗan Dawuda ne kuwa?”

24 Amma da Farisiyawa suka ji haka, sai suka ce, “Ahab, da Be’elzebub§ sarkin
aljanu ne kaɗai, wannan mutum yake fitar da aljanu.”

25 Yesu kuwa ya san tunaninsu sai ya ce musu, “Duk mulkin da yake gāba da kansa
zai lalace, kuma duk birni ko gidan da yake rabe gāba da kansa ba zai ɗore ba. 26 In
Shaiɗan yana fitar da Shaiɗan, ai, ya rabu yana gāba da kansa ke nan. Yaya kuwa
mulkinsa zai ɗore? 27 In kuwa ta wurin Be’elzebub nake fitar da aljanu, to, ta wa
mutanenku suke fitar da su? Saboda haka, su ne za su zama alƙalanku. 28 Amma in
ina fitar da aljanu ta wurin Ruhun Allah ne, to, fa, mulkin Allah ya zo muku ke nan.

29 “Ko kuwa, yaya wani zai iya shiga gidan mai ƙarfi yǎ ƙwace masa kaya ba tare
da ya fara daure mai ƙarfin nan tukuna ba? Sa’an nan zai iya washe gidansa.

30 “Wanda ba ya tare da ni, yana gāba da ni ne, kuma wanda ba ya taya ni tarawa,
watsarwa yake yi. 31 Saboda haka ina gaya muku, za a gafarta wa mutane kowane
zunubi da kuma saɓo, amma saɓo game da Ruhu, ba za a gafarta ba. 32 Duk wanda
ya zargi Ɗan Mutum, za a gafarta masa, amma duk wanda ya zargi Ruhu Mai Tsarki,
ba za a gafarta masa ba, ko a wannan zamani ko a zamani mai zuwa.

*(Luka 6.43-45)*

33 “Itace mai kyau, yakan ba da ’ya’ya masu kyau. Itace marar kyau kuma, yakan
ba da ’ya’ya marasa kyau. Itace dai, da irin ’ya’yansa ne ake gane shi. 34 Ku macizai,
ta yaya ku da kuke mugaye za ku iya magana kirki? Gama daga baki, mutum yakan
faɗi abin da yake cikin zuciya. 35 Mutumin kirki yakan fito da abubuwa masu kyau
daga ajiyar da aka a yi cikinsa, mugun mutum kuwa yakan fito da mugayen abubuwa
daga cikin muguntar da aka yi ajiya a cikinsa. 36 Amma ina gaya muku cewa mutane
za su ba da lissafi a ranar shari’a a kan kowace kalmar banza da suka faɗa. 37 Gama
ta wurin kalmominka za a kuɓutar da kai, kuma ta wurin kalmominka za a hukunta
ka.”

*Alamar Yunana*
*(Markus 8.11,12; Luka 11.29-32)*

38 Sa’an nan waɗansu Farisiyawa da malaman dokoki suka ce masa, “Malam, muna
so mu ga wata alama mai banmamaki daga gare ka.”

‡ **12:21** Ish 42.1-4 § **12:24** Da Girik Be’elzebul Ko kuwa Be’elzebul; haka ma a aya 27

39 Sai ya amsa ya ce, "Mugaye da masu zinan zamanin nan suna neman wata alama
mai banmamaki! Amma babu wadda za a nuna musu, sai dai alama ta annabi
Yunana. 40 Gama kamar yadda Yunana ya yi yini uku da kuma dare uku a cikin
wani babban kifi, haka Ɗan Mutum zai yi yini uku da kuma dare uku a cikin ƙasa.
41 Mutanen Ninebe za su tashi a ranar shari'a tare da wannan zamani, su kuwa
hukunta shi; don sun tuba saboda wa'azin Yunana, yanzu kuwa ga wanda ya fi
Yunana girma a nan. 42 Sarauniyar Sheba za tă tashi a ranar shari'a tare da wannan
zamani, tă kuwa hukunta shi; don ta zo daga ƙarshen duniya, ta saurari hikimar
Solomon, yanzu kuwa ga wanda ya fi Solomon girma a nan.

*(Luka 11.24-26)*

43 "Sa'ad da mugun ruhu ya fita daga mutum, yakan bi wuraren da ba ruwa yana
neman hutu, ba ya kuwa samu. 44 Sa'an nan yakan ce, 'Zan koma gidan da na bari.'
Sa'ad da ya iso, ya tarar da gidan ba kowa a ciki, shararre, kuma a kintse. 45 Sai
yă je yă ɗebo waɗansu ruhohi bakwai da suka fi shi mugunta, su kuwa zo su shiga
su zauna a can. Karshen mutumin nan fa zai fi farkonsa muni. Haka zai zama ga
wannan mugun zamani."

### *Mahaifiyar Yesu da 'yan'uwansa*
*(Markus 3.31-35; Luka 8.19-21)*

46 Yayinda Yesu yake cikin magana da taron, sai ga mahaifiyarsa da 'yan'uwansa
tsaye a waje, suna so su yi magana da shi. 47 Wani ya ce masa, "Mahaifiyarka da
'yan'uwanka suna tsaye a waje, suna so su yi magana da kai."*
48 Ya amsa masa ya ce, "Wace ce mahaifiyata, su wane ne kuma 'yan'uwana?" 49 Sai
ya miƙa hannu wajen almajiransa ya ce, "Ga mahaifiyata da kuma 'yan'uwana. 50 Ai,
duk wanda yake aikata nufin Ubana wanda yake cikin sama, shi ne ɗan'uwana da
'yar'uwata da kuma mahaifiyata."

# 13

### *Misalin mai shuka*
*(Markus 4.1-9; Luka 8.4-8)*

1 A ranan nan sai Yesu ya fita daga gida ya je ya zauna a bakin tafkin. 2 Taron
mutane mai yawan gaske suka taru kewaye da shi har ya kai sai da ya shiga jirgin
ruwa ya zauna, yayinda dukan mutane suka tsaya a gaci. 3 Sa'an nan ya faɗa musu
abubuwa da yawa cikin misalai, yana cewa, "Wani manomi ya fita don yă shuka
irinsa. 4 Da yana yafa irin, waɗansu suka fāffāɗi a kan hanya, tsuntsaye kuwa suka
zo suka cinye su. 5 Waɗansu suka fāɗi a wurare mai duwatsu, inda babu ƙasa sosai,
nan da nan kuwa suka tsira, da yake ƙasar ba zurfi. 6 Sai dai da rana ta ɗaga, sai tsire-
tsiren suka ƙone, suka kuma yanƙwane domin ba su da saiwa sosai. 7 Waɗansu irin
suka fāɗi a cikin ƙaya, ƙayan kuwa ta yi girma ta shaƙe su. 8 Har yanzu, waɗansu
irin suka fāffāɗi a ƙasa mai kyau, inda suka ba da amfani riɓi ɗari, sittin ko kuma
talatin na abin da aka shuka. 9 Duk mai kunnen ji, yă ji."

*(Markus 4.10-12; Luka 8.9,10)*

10 Almajiran suka zo wurinsa suka tambaye shi, "Me ya sa kake wa mutane magana
da misalai?"
11 Ya amsa ya ce, "Sanin asirin mulkin sama kam, ku aka ba wa, amma su ba a ba
su ba. 12 Duk wanda yake da shi, za a ƙara masa, zai kuwa samu a yalwace. Duk
wanda kuma ba shi da shi, ko ɗan abin da yake da shi ma, za a karɓe. 13 Abin da ya
sa nake musu magana da misalai ke nan.
"Ko da yake suna kallo, ba sa gani;

---

* **12:47** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā ba su da aya 47.

ko da yake suna saurara, ba sa ji ko su gane.
14 A kansu ne aka cika annabcin Ishaya cewa,
“ ‘Za ku yi ta ji amma ba za ku taɓa ganewa ba;
za ku yi ta kallo amma ba za ku taɓa gani ba.
15 Gama zuciyar mutanen nan ta taurare;
da ƙyar suke ji da kunnuwansu,
sun kuma rufe idanunsu.
Da ba haka ba, mai yiwuwa su gani da idanunsu,
su kuma ji da kunnuwansu,
su gane a zuciyarsu,
su kuwa juya, in kuma warkar da su.’*
16 Amma idanunku masu albarka ne domin suna gani, haka ma kunnuwanku domin
suna ji. 17 Gama gaskiya nake gaya muku, annabawa da mutane masu adalci da yawa
sun yi marmarin ganin abin da kuke gani amma ba su gani ba, su kuma ji abin da
kuke ji amma ba su ji ba.

*(Markus 4.13-20; Luka 8.11-15)*

18 “To, ku saurari ma’anar misali na mai shukan nan. 19 Duk sa’ad da wani ya ji
saƙo game da mulkin bai kuwa fahimce shi ba, mugun nan yakan zo yă ƙwace abin
da aka shuka a zuciyarsa. Wannan shi ne irin da ya fāɗi a kan hanya. 20 Wanda ya
karɓi irin da ya fāɗi a wuraren duwatsu kuwa, shi ne mutumin da yakan ji maganar,
nan da nan kuwa yă karɓe ta da murna. 21 Sai dai da yake ba shi da saiwa, yakan ɗan
jima kaɗan kawai. Da wata wahala ko tsanani ya auko masa saboda maganar, nan
da nan sai yă ja da baya. 22 Wanda ya karɓi irin da ya fāɗi cikin ƙaya kuwa, shi ne
mutumin da yakan ji maganar, sai dai damuwoyin rayuwan nan da jarrabar arzikin
duniya sukan shaƙe shi, yă sa maganar ta kāsa amfani. 23 Amma wanda ya karɓi irin
da ya fāɗi a ƙasa mai kyau, shi ne mutumin da yakan ji maganar yă kuwa fahimce
ta. Yakan ba da amfani wani riɓi ɗari, sittin, ko talatin na abin da aka shuka.”

*Misalin ciyayi*

24 Yesu ya ba su wani misali. “Mulkin sama yana kama da wani da ya shuka iri mai
kyau a cikin gonarsa. 25 Amma yayinda kowa yake barci, abokin gābansa ya zo ya
yafa ciyayi a cikin alkamar, ya tafi abinsa. 26 Sa’ad da alkamar ta tashi ta yi kawuna,
sai ciyayin ma suka bayyana.
27 “Bayin mai gonar suka zo wurinsa suka ce, ‘Ranka yă daɗe, ashe, ba iri mai kyau
ka shuka a gonarka ba? To, ina ciyayin nan suka fito?’
28 “Sai ya ce, ‘Abokin gāba ne ya yi wannan.’
“Bayin suka tambaye shi suka ce, ‘Kana so mu je mu tuttumɓuke su?’
29 “Ya amsa ya ce, ‘A’a, don kada garin tuttumɓuke ciyayi, ku cire har da alkamar.
30 Ku ƙyale su su yi girma tare sai lokacin girbi. A lokacin zan gaya wa masu girbi,
da fari ku tara ciyayin ku kuma daure su dami-dami don a ƙone; sa’an nan ku tara
alkamar ku kuma kawo su cikin rumbuna.’ ”

*Misalai na ƙwayar mustad da na yisti*
*(Markus 4.30-32; Luka 13.18-21)*

31 Ya ba su wani misali ya ce, “Mulkin sama yana kama da ƙwayar mustad, wadda
mutum ya ɗauka ya shuka a gonarsa. 32 Ko da yake ita ce mafi ƙanƙanta cikin
ƙwayoyinku, duk da haka sa’ad da ta yi girma, takan zama mafi girma cikin tsire-
tsiren lambu ta kuma zama itace, har tsuntsayen sararin sama su zo su yi sheƙa a
rassansa.”

---

* **13:15** Ish 6.9,10

33 Har yanzu ya ba su wani misali ya ce, “Mulkin sama yana kama da yisti wanda
mace ta ɗauka ta kwaɓa garin alkama mai yawa, har sai da yistin ya gauraye yistin
duka.”

*(Markus 4.33,34)*

34 Yesu ya faɗa wa taron dukan waɗannan abubuwa cikin misalai; bai faɗa musu
kome ba, sai tare da yin amfani da misalai. 35 Ta haka aka cika abin da aka faɗa ta
wurin annabi cewa,
“Zan buɗe bakina da misalai,
zan faɗi abubuwan da suke ɓoye tun halittar duniya.”†

### *An bayyana misali na ciyayi*

36 Sa’an nan ya bar taron ya shiga gida. Almajiransa kuwa suka zo wurinsa suka
ce, “Bayyana mana misalin ciyayin nan a gona.”
37 Ya amsa ya ce, “Mai yafa irin mai kyan nan, shi ne Ɗan Mutum. 38 Gonar kuwa
ita ce duniya, irin nan mai kyau kuwa suna a matsayin ’ya’yan mulkin. Ciyayin nan
kuma su ne ’ya’yan mugun nan, 39 abokin gāban da yake shuka su kuwa, Iblis ne.
Lokacin girbi kuma shi ne ƙarshen zamani, masu girbin kuwa su ne mala’iku.
40 “Kamar yadda aka tattara ciyayin aka kuma ƙone a wuta, haka zai zama a
ƙarshen zamani. 41 Ɗan Mutum zai aiki mala’ikunsa, su kuwa cire daga mulkinsa
kome da yake jawo zunubi da kuma duk masu aikata mugunta. 42 Za su jefa su cikin
wuta mai zafi, inda za a yi kuka da cizon haƙora. 43 Sa’an nan masu adalci za su
haskaka kamar rana a mulkin Ubansu. Duk mai kunnen ji, yă ji.”

### *Misalai na ɓoyayyiyar dukiya da na lu’ulu’u*

44 “Mulkin sama yana kama da dukiyar da aka ɓoye a gona. Da wani ya same ta,
sai yă sāke ɓoye ta, sa’an nan cikin farin cikinsa yă je yă sayar da duk abin da yake
da shi yă sayi gonar.
45 “Har wa yau dai, mulkin sama yana kama da ɗan kasuwa mai neman lu’ulu’ai
masu kyau. 46 Da ya sami dutse guda mai daraja sosai, sai ya tafi ya sayar da dukan
abin da yake da shi ya saye shi.

### *Misalin taru*

47 “Har yanzu, mulkin sama yana kama da abin kamun kifin da aka jefa cikin
tafki yă kamo kifi iri-iri. 48 Da abin kamun kifi ya cika, masuntan suka jawo shi
gaci. Sai suka zauna suka tattara kifi masu kyau a kwanduna, amma suka zubar da
marasa kyau. 49 Haka zai kasance a ƙarshen zamani. Mala’iku za su zo su ware masu
mugunta daga masu adalci 50 su kuma jefa su cikin wuta mai zafi, inda za a yi kuka
da cizon haƙora.”
51 Yesu ya tambaye su ya ce, “Kun gane dukan waɗannan abubuwa?”
Suka amsa, “I.”
52 Sa’an nan ya ce musu, “Saboda haka duk malamin dokokin da ya horu game
da koyarwar mulkin sama, yana kama da maigida wanda yakan fitar daga ɗakin
ajiyarsa sababbin dukiya da kuma tsofaffi.”

### *Rashin ganin darajar annabi*

*(Markus 6.1-6; Luka 4.16-30)*

53 Sa’ad da Yesu ya gama ba da waɗannan misalai, sai ya ci gaba daga can. 54 Yana
isowa garinsa, sai ya fara koya wa mutane a cikin majami’arsu, suka kuwa yi mamaki.
Suka yi ta tambaya suna cewa, “Ina wannan mutum ya sami irin wannan hikima
da kuma ayyukan banmamaki haka? 55 Wannan ba shi ne ɗan kafinta nan ba? Ba
mahaifiyarsa ba ce Maryamu, ’yan’uwansa kuma Yaƙub, Yusuf, Siman da Yahuda ba?

† **13:35** Zab 78.2

56 Duk ʼyanʼuwansa mata kuma ba tare da mu suke ba? To, a ina wannan mutum ya
sami dukan waɗannan abubuwa?" 57 Sai suka ji haushinsa.
Amma Yesu ya ce musu, "Sai a garinsa da kuma a gidansa na kaɗai annabi ba ya
samun girma."
58 Bai kuwa yi abubuwan banmamaki da yawa a can ba saboda rashin bangaski-
yarsu.

# 14

### *An yanke kan Yohanna Mai Baftisma*
### *(Markus 6.14-29; Luka 9.7-9)*

1 A lokacin nan sarki Hiridus ya ji labarin Yesu, 2 sai ya ce wa fadawansa, "Wannan
Yohanna Mai Baftisma ne; ya tashi daga matattu! Shi ya sa abubuwan banmamakin
nan suke faruwa ta wurinsa."
3 To, dā Hiridus ya kama Yohanna ya daure, ya kuma sa shi cikin kurkuku saboda
Hiridiyas, matar ɗanʼuwansa Filibus, 4 gama Yohanna ya dinga ce masa, "Ba daidai
ba ne ka aure ta." 5 Hiridus ya so yǎ kashe Yohanna, amma yana jin tsoron mutane,
don sun ɗauka shi annabi ne.
6 A bikin tuna da ranar haihuwar Hiridus, diyar Hiridiyas ta yi musu rawa ta kuma
gamsar da Hiridus ƙwarai, 7 har ya yi alkawari da rantsuwa cewa zai ba ta duk abin
da ta roƙa. 8 Da mahaifiyarta ta zuga ta, sai ta ce, "Ba ni a cikin kwanon nan, kan
Yohanna Mai Baftisma." 9 Sarki ya yi baƙin ciki, amma saboda rantsuwarsa da kuma
baƙinsa, sai ya ba da umarni a ba ta abin da ta roƙa 10 ya kuma sa aka yanke kan
Yohanna a kurkuku. 11 Aka kawo kansa cikin kwano aka ba yarinyar, ita kuma ta
kai wa mahaifiyarta. 12 Almajiran Yohanna suka zo suka ɗauki gawarsa suka binne.
Saʼan nan suka je suka gaya wa Yesu.

### *Yesu ya ciyar da dubu biyar*
### *(Markus 6.30-44; Luka 9.10-17; Yohanna 6.1-14)*

13 Saʼad da Yesu ya ji abin da ya faru, sai ya shiga jirgin ruwa ya janye shi kaɗai
zuwa wani wuri inda ba kowa. Da jin haka, taron mutane suka bi shi da ƙafa daga
garuruwa. 14 Da Yesu ya sauka ya kuma ga taro mai yawa, sai ya ji tausayinsu ya
kuma warkar da marasa lafiyarsu.
15 Da yamma ta yi, sai almajiransa suka zo wurinsa suka ce, "Wurin nan fa ba
kowa, ga shi kuma rana ta kusa fāɗuwa. Ka sallami taron don su shiga ƙauyuka su
nemi wa kansu abinci."
16 Yesu ya amsa, "Ba su bukata su tafi. Ku ku ba su wani abu su ci."
17 Suka ce, "Burodi biyar da kifi biyu ne kawai muke da su a nan."
18 Ya ce, "Ku kawo mini su a nan." 19 Sai ya umarci mutanen su zazzauna a kan
ciyawa. Da ya ɗauki burodi biyar da kifin biyun nan ya dubi sama, ya yi godiya
ya kuma kakkarya burodin. Saʼan nan ya ba wa almajiransa, almajiran kuwa suka
ba wa mutane. 20 Duk suka ci suka ƙoshi, almajiran kuwa suka kwashe ragowar
gutsattsarin cike da kwanduna goma sha biyu. 21 Yawan waɗanda suka ci, sun yi
wajen maza dubu biyar, ban da mata da yara.

### *Yesu ya yi tafiya a kan ruwa*
### *(Markus 6.45-52; Yohanna 6.15-21)*

22 Nan da nan Yesu ya sa almajiran su shiga jirgin ruwa su sha gabansa, su haye
zuwa ɗayan hayin, yayinda shi kuma yǎ sallami taron. 23 Bayan ya sallame su, sai ya
haura bisan gefen dutse shi kaɗai don yǎ yi adduʼa. Da yamma ta yi, yana can shi
kaɗai, 24 jirgin ruwan kuwa ya riga ya yi nesa da gaci, yana fama da raƙuman ruwa
domin iska tana gāba da shi.

25 Wajen tsaro na huɗu na dare, sai Yesu ya nufe su, yana takawa a kan tafkin.
26 Sa'ad da almajiran suka gan shi yana takawa a kan tafkin, sai tsoro ya kama su.
Suka yi ihu don tsoro suka ce, "Fatalwa ce."
27 Amma nan da nan Yesu ya ce musu, "Ku yi ƙarfin hali! Ni ne. Kada ku ji tsoro."
28 Sai Bitrus ya amsa ya ce, "Ubangiji in kai ne ka ce mini in zo wurinka a kan
ruwan."
29 Ya ce, "Zo."
Sai Bitrus ya fita daga jirgin ruwan, ya taka a kan ruwan ya nufe wajen Yesu.
30 Amma da ya ga haukar iskar, sai ya ji tsoro, ya kuma fara nutsewa, sai ya yi ihu
ya ce, "Ubangiji, ka cece ni!"
31 Nan da nan Yesu ya miƙa hannu ya kamo shi ya ce, "Kai mai ƙarancin
bangaskiya, don me ka yi shakka?"
32 Da suka hau jirgin ruwan, sai iskar ta kwanta. 33 Waɗanda suke cikin jirgin
ruwan kuwa suka yi masa sujada, suna cewa, "Gaskiya kai Ɗan Allah ne."

*(Markus 6.45-52; Yohanna 6.15-21)*

34 Sa'ad da suka haye, sai suka sauka a Gennesaret. 35 Da mutanen wurin suka gane
da Yesu, sai suka kai labari a ko'ina a ƙauyukan da suke kewaye. Mutane suka kawo
masa dukan marasa lafiyarsu 36 suka kuwa roƙe shi yǎ bar marasa lafiya su taɓa ko
da gefen rigarsa kawai, duk waɗanda suka taɓa shi kuwa suka warke.

# 15

*Mai tsabta da marar tsabta*
*(Markus 7.1-13)*

1 Sa'an nan waɗansu Farisiyawa da malaman dokoki suka zo wurin Yesu daga
Urushalima suka yi tambaya suka ce, 2 "Me ya sa almajiranka suke karya al'adun
dattawa? Ba sa wanke hannuwansu kafin su ci abinci!"
3 Yesu ya amsa ya ce, "Ku ma me ya sa kuke karya dokar Allah saboda al'adarku?
4 Gama Allah ya ce, 'Ka girmama mahaifinka da mahaifiyarka,*kuma duk wanda ya
zagi mahaifinsa ko mahaifiyarsa dole a kashe shi.'† 5 Amma ku kukan ce, in wani
ya ce wa mahaifinsa ko mahaifiyarsa, 'Duk taimakon da dā ya kamata za ku samu
daga gare ni an ba wa Allah,' 6 ba zai 'girmama mahaifinsa' da shi ba. Ta haka kun
yi banza da maganar Allah saboda al'adarku. 7 Ku munafukai! Daidai ne Ishaya ya
yi annabci a kanku da ya ce,
8 " 'Waɗannan mutane da baki kawai suke girmama ni,
amma zukatansu suna nesa da ni.
9 A banza suke mini sujada,
koyarwarsu, dokoki ne kawai da mutane suke koyarwa.' "‡

*(Markus 7.14-23)*

10 Sai Yesu ya kira taron wurinsa ya ce, "Ku saurara ku kuma gane. 11 Abin da yake
shiga bakin mutum ba ya ƙazantar da shi, sai dai abin da yake fitowa daga bakinsa,
shi ne yake ƙazantar da shi."
12 Sai almajiran suka zo wurinsa suka ce, "Ka san cewa Farisiyawa ba su ji daɗi
sa'ad da suka ji wannan ba?"
13 Ya amsa ya ce, "Duk tsiron da Ubana na sama bai shuka ba, za a tumɓuke shi
daga saiwoyi. 14 Ku ƙyale su, ai, makafin jagorai ne.§In makaho ya yi wa makaho
jagora, dukansu za su fāɗa a rami."
15 Bitrus ya ce, "Ka bayyana mana wannan misali."

* **15:4** Fit 20.12; M Sh 5.16 † **15:4** Fit 21.17; Fir 20.9 ‡ **15:9** Ish 29.13 § **15:14** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da jagorai ne na makafi

16 Yesu ya tambaye su ya ce, “Har yanzu ba ku gane ba ne? 17 Ba ku gane cewa
duk abin da ya shiga baki yakan wuce ciki ne daga nan kuma yǎ fita daga jiki ba?
18 Amma abubuwan da suke fitowa ta baki suna fitowa ne daga zuciya, su ne kuma
suke ƙazantar da mutum. 19 Gama daga zuciya ne mugayen tunani, kisankai, zina,
fasikanci, sata, shaidar ƙarya, ɓatan suna, suka fitowa. 20 Waɗannan su ne suke
ƙazantar da mutum; amma cin abinci ba tare da wanke hannuwa ba, ba ya ƙazantar
da mutum.”

### *Bangaskiyar mutuniyar Kan’ana*
*(Markus 7.24-30)*

21 Barin wurin ke nan, sai Yesu ya janye zuwa yankin Taya da Sidon. 22 Wata
mutuniyar Kan’ana daga wajajen ta zo wurinsa, tana ihu tana cewa, “Ubangiji, Ɗan
Dawuda, ka yi mini jinƙai! ’Yata tana shan wahala ƙwarai daga aljanin da yake
cikinta.”

23 Yesu bai ce mata uffam ba. Saboda haka almajiransa suka zo wurinsa suka roƙe
shi suka ce, “Ka kore ta tǎ tafi, tana ta binmu tana damunmu da ihu.”

24 Ya amsa ya ce, “An aiko ni wurin ɓatattun tumakin Isra’ila ne kaɗai.”

25 Sai macen ta zo ta durƙusa a gabansa ta ce, “Ubangiji, ka taimake ni!”

26 Ya amsa ya ce, “Ba daidai ba ne a ɗauki abincin yara a jefa wa karnukansu.”

27 Ta amsa, ta ce, “I, Ubangiji, amma karnuka ma sukan ci gutsattsarin da sukan
fāɗi daga teburin maigidansu.”

28 Sa’an nan Yesu ya amsa ya ce, “Mace, kina da bangaskiya mai yawa! An biya
miki bukatarki.” ’Yarta kuwa ta warke nan take.

### *Yesu ya ciyar da dubu huɗu*

29 Yesu ya tashi daga nan ya bi ta gefen Tekun Galili. Sa’an nan ya haura gefen wani
dutse ya zauna. 30 Taron mutane mai girma kuwa suka zo wurinsa, suna kawo masa
guragu, makafi, shanyayyu, kurame da dai waɗansu da yawa, suka kuwa kwantar
da su a gabansa; ya kuma warkar da su. 31 Mutanen kuwa suka yi mamaki sa’ad da
suka ga kurame suna magana, shanyayyu suna samun lafiya, guragu suna takawa,
makafi kuma suna ganin gari. Sai suka yabi Allah na Isra’ila.

*(Markus 8.1-10)*

32 Yesu ya kira almajiransa wurinsa ya ce, “Ina jin tausayin mutanen nan; gama
kwana uku ke nan suke tare da ni ba abin da za su ci. Ba na so in sallame su da
yunwa, don kada su kāsa a hanya.”

33 Sai almajiransa suka amsa suka ce, “Ina za mu sami isashen burodi a wannan
wurin da babu kowa mu ciyar da irin taron nan?”

34 Yesu ya tambaye su, “Burodi guda nawa kuke da shi?”

Suka amsa suka ce, “Guda bakwai da ’yan ƙananan kifaye.”

35 Ya sa taron su zazzauna a ƙasa. 36 Sa’an nan ya ɗauki burodi guda bakwai da
kuma kifayen nan, da ya yi godiya, sai ya kakkarya su ya ba wa almajiran, su kuma
suka ba wa mutane. 37 Duk kuwa suka ci, suka ƙoshi. Daga baya almajiran suka
kwashe ragowar gutsattsarin cike da kwanduna bakwai. 38 Yawan waɗanda suka ci
kuwa, maza dubu huɗu ne, ban da mata da yara. 39 Bayan Yesu ya sallami taron, sai
ya shiga jirgin ruwa ya tafi wajajen Magadan.

## 16

### *Neman alama*
*(Markus 8.11-13; Luka 12.54-56)*

1 Farisiyawa da Sadukiyawa suka zo don su gwada Yesu ta wurin neman yǎ nuna
musu wata alama daga sama.

2 Ya amsa ya ce,* "Sa'ad da yamma ta yi, kukan ce, 'Yanayi zai yi kyau, gama sararin
sama ya yi ja,' 3 da safe kuma, ku ce, 'Yau kam za a yi hadari, gama sararin sama
ya yi ja, ya kuma ɓata fuska.' Kun san yadda za ku fassara yanayin sararin sama,
amma ba kwa iya fassarar alamun lokuta. 4 Wannan mugu da mazinacin zamani
yana neman wani abin banmamaki, amma ba wata alamar da za a nuna wa wannan
zamani sai dai ta Yunana." Sai Yesu ya bar su ya tafi abinsa.

*Yistin Farisiyawa da Sadukiyawa*
*(Markus 8.14-21)*

5 Da suka ƙetare tafkin, almajiran sun manta su riƙe burodi. 6 Yesu ya ce musu,
"Ku yi hankali, ku yi taka zallan da yistin Farisiyawa da Sadukiyawa."
7 Sai suka fara tattaunawa da junansu suna cewa, "Ko don ba mu kawo burodi ba
ne."
8 Sane da abin da suke zance, sai Yesu ya ce, "Ku masu ƙarancin bangaskiya, don me
kuke magana da junanku a kan ba ku zo da burodi ba? 9 Har yanzu ba ku gane ba ne?
Ba ku tuna da gurasa biyar ɗin nan na mutum dubu biyar ba? Kwando nawa kuka
tattara cike? 10 Ko kuma burodi bakwai nan na mutum dubu huɗu, cikakku manyan
kwanduna nawa kuka ɗauka? 11 Yaya kuka kāsa gane cewa ba zancen burodi nake
yi ba? Sai dai ku yi hankali da yistin Farisiyawa da Sadukiyawa." 12 Sa'an nan suka
gane ba cewa yake musu su yi hankali da yistin da ake amfani da shi a burodi ba ne,
sai dai su yi hankali da koyarwar Farisiyawa da Sadukiyawa ne.

*Shaidar Bitrus a kan Kiristi*
*(Markus 8.27-30; Luka 9.18-21)*

13 Sa'ad da Yesu ya zo yankin Kaisariya Filibbi, sai ya tambayi almajiransa ya ce,
"Wa mutane suke ce da Ɗan Mutum?"
14 Suka amsa, "Waɗansu suna ce Yohanna Mai Baftisma; waɗansu kuma suna
ce annabi Iliya; har wa yau waɗansu suna ce Irmiya ne ko kuma ɗaya daga cikin
annabawa."
15 Ya tambaye su, "Amma ku fa, wane ne ni a ganinku?"
16 Siman Bitrus ya amsa ya ce, "Kai ne Kiristi,† Ɗan Allah mai rai."
17 Yesu ya amsa ya ce, "Mai albarka ne kai Siman ɗan Yunana, gama ba mutum
ne ya bayyana maka wannan ba, sai dai Ubana da yake cikin sama. 18 Ina kuwa
gaya maka, kai ne Bitrus,‡ a kan wannan dutse zan gina ikkilisiyata, kuma ƙofofin
Hades§ ba za su rinjaye ta ba. 19 Zan ba ka mabuɗan mulkin sama; kome ka daure a
duniya zai zama a daure a sama, kome kuma ka kunce a duniya zai zama a kunce
a sama." 20 Sa'an nan ya gargaɗe almajiransa cewa kada su faɗa wa kowa shi ne
Kiristi.

*Yesu ya yi zancen mutuwarsa*
*(Markus 8.31–9.1; Luka 9.22-27)*

21 Tun daga wannan lokaci Yesu ya fara bayyana wa almajiransa cewa dole yă tafi
Urushalima yă sha wahaloli da yawa a hannun dattawa, manyan firistoci da kuma
malaman dokoki, dole a kashe shi, a rana ta uku kuma a tashe shi.
22 Bitrus ya ja shi gefe ya fara tsawata masa yana cewa, "Sam, Ubangiji! Wannan
ba zai taɓa faruwa da kai ba!"
23 Yesu ya juya ya ce wa Bitrus, "Rabu da ni, Shaiɗan! Kai abin sa tuntuɓe ne a
gare ni; ba ka tunanin al'amuran Allah, sai dai al'amuran mutane."
24 Sa'an nan Yesu ya ce wa almajiransa, "Duk mai son bina, dole yă ƙi kansa, yă
ɗauki gicciyensa, yă bi ni. 25 Gama duk mai son ceton ransa zai rasa shi, amma duk

* **16:2** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na farko-farko ba su da raguwar aya 2 da kuma dukan aya 3 † **16:16** Ko kuwa a Almasihu; haka ma a aya 20 ‡ **16:18** Bitrus yana nufin dutse. § **16:18** Ko kuwa a lahira

wanda ya rasa ransa saboda ni, zai same shi. 26 Me mutum zai amfana in ya sami
duniya duka, amma ya rasa ransa? Ko kuwa me mutum zai bayar a bakin ransa?
27 Gama Ɗan Mutum zai zo cikin ɗaukakar Ubansa, tare da mala’ikunsa, sa’an nan
zai ba wa kowane mutum lada gwargwadon abin da ya yi.
28 “Gaskiya nake gaya muku, akwai waɗansu da suke tsaitsaye a nan da ba za su
mutu ba sai sun ga Ɗan Mutum yana zuwa cikin mulkinsa.”

# 17

### *Sākewar kamanni*
*(Markus 9.2-13; Luka 9.28-36)*

1 Bayan kwana shida, sai Yesu ya ɗauki Bitrus, Yaƙub da Yohanna ɗan’uwan Yaƙub,
ya kai su kan wani dutse mai tsawo, su kaɗai. 2 A can aka sāke kamanninsa a gabansu.
Fuskarsa ta haskaka kamar rana, tufafinsa kuwa suka zama fari fat suna walƙiya.
3 Nan take sai ga Musa da Iliya suka bayyana a gabansu, suna magana da Yesu.
4 Sai Bitrus ya ce wa Yesu, “Ubangiji, ya yi kyau da muke nan. In kana so, sai in
kafa bukkoki uku, ɗaya dominka, ɗaya domin Musa, ɗaya kuma domin Iliya.”
5 Yayinda yake cikin magana, sai wani girgije mai haske ya rufe su, sai wata murya
daga cikin girgijen ta ce, “Wannan Ɗana ne, wanda nake ƙauna; wanda kuma nake
jin daɗinsa ƙwarai. Ku saurare shi!”
6 Sa’ad da almajiran suka ji haka, sai suka fāɗi ƙasa rubda ciki, a firgice. 7 Amma
Yesu ya zo ya taɓa su ya ce, “Ku tashi, kada ku ji tsoro.” 8 Da suka ɗaga kai, ba su ga
kowa ba sai Yesu kaɗai.
9 Suna cikin gangarowa daga dutsen ke nan, sai Yesu ya umarce su cewa, “Kada ku
faɗa wa kowa abin da kuka gani, sai bayan an tā da Ɗan Mutum daga matattu.”
10 Almajiran suka tambaye shi suka ce, “To, me ya sa malaman dokoki suke cewa,
dole sai Iliya ya fara zuwa?”
11 Yesu ya amsa ya ce, “Tabbatacce, Iliya zai zo, zai kuma gyara dukan abubuwa.
12 Amma ina faɗa muku, Iliya ya riga ya zo, ba su kuwa gane shi ba, amma suka yi
masa duk abin da suka ga dama. Haka ma Ɗan Mutum zai sha wahala a hannunsu.”
13 Sa’an nan almajiran suka gane cewa yana musu zancen Yohanna Mai Baftisma ne.

### *Warkarwar yaro mai aljani*
*(Markus 9.14-29; Luka 9.37-43)*

14 Da suka isa wajen taron, sai wani mutum ya zo ya durƙusa a gabansa. 15 Ya ce,
“Ubangiji, ka yi wa ɗana jinƙai. Yana da farfaɗiya yana kuma shan wahala ƙwarai.
Ya sha fāɗuwa cikin wuta ko ruwa. 16 Na kuma kawo shi wurin almajiranka, amma
ba su iya warkar da shi ba.”
17 Yesu ya amsa ya ce, “Ya ku zamani marasa bangaskiya da kuma masu taurinkai,
har yaushe zan kasance tare da ku? Har yaushe kuma zan yi haƙuri da ku? Kawo
mini yaron a nan.” 18 Yesu ya tsawata wa aljanin, ya kuwa rabu da yaron, nan take
yaron ya warke.
19 Sa’an nan almajiran suka zo wurin Yesu a ɓoye suka tambaye shi suka ce, “Me
ya sa ba mu iya fitar da aljanin ba?”
20 Ya amsa ya ce, “Saboda kuna da ƙarancin bangaskiya sosai. Gaskiya nake gaya
muku, in kuna da bangaskiyar da take ƙanƙanuwa kamar ƙwayar mustad, za ku iya
ce wa wannan dutse, ‘Matsa daga nan zuwa can,’ zai kuwa matsa. Babu abin da zai
gagare ku.”*

*(Markus 9.30-32; Luka 9.43-45)*

* **17:20** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da kai. 21 Amma irin wannan ba ya fita, sai da addu’a da azumi

22 Da suka taru a Galili, sai ya ce musu, "Za a bashe Ɗan Mutum, a hannun mutane.
23 Za su kashe shi, a rana ta uku kuma za a tashe shi." Almajiran kuwa suka cika da
baƙin ciki.

*Harajin haikali*

24 Bayan Yesu da almajiransa suka isa Kafarnahum, sai masu karɓan harajin rabin
shekel suka zo wurin Bitrus suka ce, "Malaminku ba ya biyan harajin haikali ne†?"
25 Ya amsa ya ce "I, yana biya."
Da Bitrus ya shiga gida, Yesu ne ya fara magana. Ya ce masa, "Me ka gani, Siman?
Daga wurin wane ne sarakunan duniya suke karɓar kuɗin shiga da kuma haraji,
daga wurin 'ya'yansu ne ko kuwa daga wurin waɗansu?"
26 Bitrus ya amsa ya ce, "Daga wurin waɗansu."
Yesu ya ce masa, "Wato, an ɗauke wa 'ya'yan ke nan. 27 Amma don kada mu ɓata
musu rai, ka je tafki ka jefa ƙugiyarka. Ka ɗauki kifin da ka fara kama; ka buɗe
bakinsa, za ka sami shekel guda. Ka kawo ka ba su, harajina da naka ke nan."

# 18

*Mafi girma a mulkin sama*
*(Markus 9.33-37; Luka 9.46-48)*

1 A lokacin nan sai almajirai suka zo wurin Yesu suka yi tambaya suka ce, "Wane
ne mafi girma a mulkin sama?"
2 Sai ya kira ƙaramin yaro ya sa shi yă tsaya a tsakiyarsu. 3 Sai ya ce, "Gaskiya
nake gaya muku, in ba kun canja kuka zama kamar ƙananan yara ba, labudda, ba za
ku shiga mulkin sama ba. 4 Saboda haka, duk wanda ya ƙasƙantar da kansa kamar
wannan yaro, shi ne mafi girma a mulkin sama. 5 Duk kuma wanda ya karɓi ƙaramin
yaro kamar wannan a cikin sunana ya karɓe ni ne.

*(Markus 9.42-48; Luka 17.1,2)*

6 "Amma duk wanda ya sa ɗaya daga cikin ƙananan nan da suka gaskata da ni ya yi
zunubi, zai fiye masa a rataya babban dutsen niƙa a wuyarsa, a kuma nutsar da shi a
zurfin teku. 7 Kaiton duniya saboda abubuwan da suke sa mutane su yi zunubi! Dole
irin waɗannan abubuwa su zo, sai dai kaiton mutumin da ya zama sanadin kawo
su! 8 In hannunka ko ƙafarka yana sa ka zunubi, yanke shi ka yar. Zai fiye maka ka
shiga rai da hannu ko ƙafa ɗaya da hannuwa biyu ko ƙafafu biyu da a jefar da kai
cikin madawwamiyar wuta da hannuwa biyu ko ƙafafu biyu. 9 In kuma idonka yana
sa ka zunubi, ƙwaƙule shi ka yar. Zai fiye maka ka shiga rai da ido ɗaya, da ka shiga
jahannama ta wuta da idanunka biyu.

*Misalin ɓatacciyar tunkiya*
*(Luka 15.3-7)*

10 "Ku lura, kada ku rena ɗaya daga cikin waɗannan ƙanana. Gama ina faɗa muku
mala'ikunsu a sama kullum suna duban fuskar Ubana da yake cikin sama.*
12 "Me kuka gani? In wani yana da tumaki ɗari, sai ɗaya daga cikinsu ta ɓace, ba
sai yă bar tasa'in da taran a kan tuddai yă je neman guda ɗayan da ta ɓace ba? 13 In
kuwa ya same ta, ina gaya muku gaskiya, zai yi murna saboda ɗayan fiye da tasa'in
da taran da ba su ɓace ba. 14 Haka ma Ubanku da yake cikin sama ba ya so ko ɗaya
daga cikin ƙananan nan yă ɓace.

*Ɗan'uwa da ya yi maka laifi*
*(Luka 17.3)*

† **17:24** da Girik darik biyu * **18:10** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da sama. 11 Ɗan Mutum ya zo ne domin yă ceci abin da ya ɓata

15 “In ɗan’uwanka ya yi maka laifi, ka je ka nuna masa laifinsa, tsakaninku biyu
kaɗai. In ya saurare ka, ka maido da ɗan’uwanka ke nan. 16 Amma in bai saurare
ka ba, ka je tare da mutum ɗaya ko biyu, domin ‘a tabbatar da kowace magana a
bakin shaidu biyu ko uku.’† 17 In kuwa ya ƙi yă saurare su, sai ka gaya wa ikkilisiya;
in kuma ya ƙi yă saurari ikkilisiya ma, ka yi da shi kamar marar sanin Allah ko mai
karɓar haraji.
18 “Gaskiya nake gaya muku, duk abin da kuka daure a duniya, za a daure a sama,
duk kuma abin da kuka kunce a duniya, za a kunce shi a sama.
19 “Har wa yau, ina gaya muku cewa in mutum biyu a cikinku a duniya suka yarda
su roƙi wani abu, Ubana da yake cikin sama zai yi muku. 20 Gama inda mutum biyu
ko uku suka taru cikin sunana, a can ma ina tare da su.”

*Misalin bawa marar tausayi*

21 Sai Bitrus ya zo wurin Yesu ya yi masa tambaya ya ce, “Ubangiji, sau nawa zan
yafe wa ɗan’uwana sa’ad da ya yi mini zunubi? Har sau bakwai?”
22 Yesu amsa ya ce, “Ina gaya maka, ba sau bakwai ba, amma sau saba’in da
bakwai.‡
23 “Saboda haka, mulkin sama yana kama da wani sarki wanda ya so yă yi
ƙididdigar dukiyarsa da take a hannun bayinsa. 24 Da ya fara ƙididdigar, sai aka
kawo masa wani wanda yake bin bashin talenti dubu goma. 25 Da yake bai iya biya
ba, sai maigida ya umarta a sayar da shi da matarsa da yaransa da kuma duk abin
da yake da shi, a biya bashin.
26 “Bawan ya durƙusa a gabansa. Ya yi roƙo ya ce, ‘Ka yi mini haƙuri, zan biya ka
ƙaf.’ 27 Maigidan bawan ya ji tausayinsa, ya yafe masa bashin, ya kuma sake shi.
28 “Amma da wannan bawa ya fita, sai ya gamu da wani abokin bautarsa wanda
yake binsa bashin dinari ɗari. Sai ya cafke shi, ya shaƙe shi a wuya yana cewa, ‘Biya
ni abin da nake binka!’
29 “Wannan abokin bautarsa ya durƙusa ya roƙe shi, ‘Ka yi mini haƙuri, zan biya
ka.’
30 “Amma ya ƙi. A maimako, sai ya je ya sa aka jefa shi a kurkuku, har yă biya
bashin. 31 Sa’ad da sauran bayin suka ga abin da ya faru, abin ya ɓata musu rai
ƙwarai, sai suka tafi suka faɗa wa maigidansu dukan abin da ya faru.
32 “Sai maigidan ya kira wannan bawa. Ya ce, ‘Kai mugun bawa, na yafe duk bashin
da nake binka domin ka roƙe ni. 33 Ashe, bai kamata kai ma ka ji tausayin abokin
bautarka yadda na yi maka ba?’ 34 Cikin fushi, maigidan ya miƙa shi ga ma’aikatan
kurkuku su gwada masa azaba, har yă biya dukan bashin da ake binsa.
35 “Haka Ubana da yake cikin sama zai yi da kowannenku, in ba ku yafe wa
’yan’uwanku daga zuciyarku ba.”

# 19

*Kashen aure*
*(Markus 10.1-12)*

1 Sa’ad da Yesu ya gama faɗin waɗannan abubuwa, sai ya bar Galili, ya tafi yankin
Yahudiya a ɗaya gefen Urdun. 2 Taron mutane mai yawa suka bi shi, ya kuwa warkar
da su a can.
3 Waɗansu Farisiyawa suka zo wurinsa don su gwada shi. Suka yi tambaya suka ce,
“Daidai ne mutum yă saki matarsa saboda wani dalili da kuma a kan kowane dalili?”
4 Ya amsa ya ce, “Ba ku taɓa karantawa ba ne cewa, a farkon halitta, Mahalicci
‘ya yi su namiji da ta mace,’* 5 ya kuma ce, ‘Saboda wannan dalili, namiji zai bar

† **18:16** M Sh 19.15 ‡ **18:22** Ko kuwa saba’in sau bakwai * **19:4** Far 1.27

mahaifinsa da mahaifiyarsa yă manne wa matarsa, biyun kuwa su zama jiki guda'?†
6 Ta haka, ba sa ƙara zama biyu, sai dai ɗaya. Saboda haka abin da Allah ya haɗa fa,
kada mutum yă raba."
7 Suka yi tambaya, suka ce, "To, me ya sa Musa ya umarta cewa mutum yă ba wa
matarsa takardar saki, yă kuma kore ta?"
8 Yesu ya amsa ya ce, "Musa ya ba ku izini ku saki matanku saboda taurin zuciyarku
ne. Amma ba haka yake ba daga farko. 9 Ina faɗa muku cewa duk wanda ya saki
matarsa, sai dai a kan rashin aminci a cikin aure, ya kuwa auri wata, ya yi zina ke
nan."
10 Almajiran suka ce masa, "In haka yake tsakanin miji da mata, ashe, ya ma fi
kyau kada a yi aure."
11 Yesu ya ce, "Ba kowa ba ne zai yarda da wannan magana, sai dai waɗanda aka
yarda musu. 12 Gama waɗansu bābānni ne domin haka aka haife su; waɗansu kuwa
mutane ne suka mai da su haka; waɗansu kuma sun ƙi aure ne saboda mulkin sama.
Duk mai iya ɗaukar wannan yă ɗauka."

### *Yesu da ƙananan yara*
### *(Markus 10.13-16; Luka 18.15-17)*

13 Sa'an nan aka kawo yara ƙanana wurin Yesu don yă ɗibiya musu hannuwansa,
yă kuma yi musu addu'a. Amma almajirai suka tsawata wa waɗanda suka kawo su.
14 Yesu ya ce, "Ku bar yara ƙanana su zo wurina, kada ku hana su, gama mulkin
sama na irin waɗannan ne." 15 Sa'ad da ya ɗibiya musu hannuwansa, sai ya tafi
abinsa.

### *Saurayi mai arziki*
### *(Markus 10.17-31; Luka 18.18-30)*

16 To, fa, sai ga wani ya zo wurin Yesu ya tambaye shi ya ce, "Malam, wane abu
mai kyau ne ya zama mini dole in yi don in sami rai madawwami?"
17 Yesu ya amsa ya ce, "Don me kake tambayata game da abin da yake mai kyau?
Akwai Mai kyau Ɗaya kaɗai. In kana so ka sami rai madawwami, ka kiyaye dokokin
nan."
18 Mutumin ya yi tambaya ya ce, "Waɗanne?"
Yesu ya amsa ya ce, " 'Kada ka yi kisankai, kada ka yi zina, kada ka yi sata, kada
ka yi shaidar ƙarya, 19 ka girmama mahaifinka da mahaifiyarka,'‡ka kuma 'ƙaunaci
maƙwabcinka kamar kanka.'§"
20 Saurayin ya ce, "Duk waɗannan na kiyaye. Me kuma ya rage mini?"
21 Yesu ya amsa ya ce, "In kana so ka zama cikakke, ka je, ka sayar da dukan
dukiyarka ka kuma ba matalauta, za ka kuwa sami dukiya a sama. Sa'an nan ka zo,
ka bi ni."
22 Da saurayin ya ji haka, sai ya tafi rai a ɓace, don yana da arziki sosai.
23 Sa'an nan Yesu ya ce wa almajiransa, "Gaskiya nake gaya muku, yana da wuya
mai arziki yă shiga mulkin sama. 24 Har wa yau ina gaya muku, zai fi sauƙi raƙumi
yă shiga ta kafar allura, da mai arziki yă shiga mulkin Allah."
25 Sa'ad da almajiran suka ji wannan, sai suka yi mamaki ƙwarai. Suka yi tambaya
suka ce, "To, wa zai sami ceto ke nan?"
26 Yesu ya kalle su ya ce, "Ga mutum kam, wannan ba ya yiwuwa, amma ga Allah
kuwa, dukan abubuwa masu yiwuwa ne."
27 Sai Bitrus ya amsa masa, "Ga shi mun bar kome don mu bi ka! Me za mu samu
ke nan?"
28 Yesu ya ce musu, "Gaskiya nake gaya muku, a lokacin sabunta dukan kome, sa'ad
da Ɗan Mutum ya zauna a kan kursiyinsa mai daraja, ku da kuka bi ni, ku ma za ku

† **19:5** Far 2.24 ‡ **19:19** Fit 20.12-16; M Sh 5.16-20 § **19:19** Fir 19.18

zauna a kan kursiyoyi goma sha biyu, kuna yi wa kabilu goma sha biyu na Isra’ila
shari’a. 29 Duk kuma wanda ya bar gidaje ko ’yan’uwa maza ko ’yan’uwa mata ko
mahaifi ko mahaifiya ko yara ko gonaki, saboda ni, zai sami abin da ya fi haka riɓi
ɗari, yǎ kuma gāji rai madawwami. 30 Amma da yawa da suke na farko, za su zama
na ƙarshe, da yawa kuma da suke na ƙarshe, za su zama na farko.

# 20

### *Misalin ma’aikata a gonar inabi*

1 “Mulkin sama yana kama da wani mai gona, wanda ya fita da sassafe don yǎ yi
hayar mutane su yi aiki a gonar inabinsa. 2 Ya yarda yǎ biya su dinari guda a yini,
sai ya tura su gonar inabinsa.

3 “Wajen sa’a ta uku, ya fita sai ya ga waɗansu suna tsattsaye a bakin kasuwa ba
sa kome. 4 Ya ce musu, ‘Ku ma ku tafi gonar inabina ku yi aiki, zan kuwa biya ku
abin da ya dace.’ 5 Saboda haka suka tafi.

“Ya sāke fita a sa’a ta shida da kuma sa’a ta tara, ya sāke yin haka. 6 Wajen sa’a
ta goma sha ɗaya, ya sāke fita, ya tarar da waɗansu har yanzu suna tsattsaye. Ya
tambaye su, ‘Don me kuke yini tsattsaye a nan ba kwa kome?’

7 “Suka amsa, ‘Don ba wanda ya ɗauke mu aiki.’

“Ya ce musu, ‘Ku ma ku je ku yi aiki a gonar inabina.’

8 “Sa’ad da yamma ta yi, sai mai gonar inabin ya ce wa wakilinsa, ‘Kira ma’aikatan,
ka biya su hakkin aikinsu, fara daga waɗanda aka ɗauke su a ƙarshe har zuwa na
farko.’

9 “Ma’aikatan da ka ɗauka wajen sa’a ta goma sha ɗaya suka zo, kowannensu kuwa
ya karɓi dinari guda. 10 Saboda haka da waɗanda aka ɗauka da fari suka zo, sun zaci
za su sami fiye da haka. Amma kowannensu ma ya karɓi dinari guda. 11 Sa’ad da
suka karɓa, sai suka fara yin gunaguni a kan mai gonar. 12 Suna cewa, ‘Waɗannan
mutanen da aka ɗauka a ƙarshe sun yi aikin sa’a ɗaya ne kawai, ka kuma mai da su
daidai da mu da muka yini muna faman aiki, muka kuma sha zafin rana.’

13 “Amma ya amsa wa ɗayansu ya ce, ‘Aboki, ban cuce ka ba. Ba ka yarda ka yi aiki
a kan dinari guda ba? 14 Ka karɓi hakkinka ka tafi. Ni na ga damar ba waɗannan na
ƙarshe daidai da yadda na ba ka. 15 Ba ni da ikon yin abin da na ga dama da kuɗina
ne? Ko kana kishi saboda ni mai kyauta ne?’

16 “Saboda haka fa, na ƙarshe za su zama na farko, na farko kuma su zama na
ƙarshe.”

### *Yesu ya sāke yin zancen mutuwarsa*
### *(Markus 10.32-34; Luka 18.31-34)*

17 To, da Yesu yana haurawa zuwa Urushalima, sai ya ja almajiran nan goma sha
biyu gefe, ya ce musu, 18 “Za mu haura zuwa Urushalima, za a kuma bashe Ɗan
Mutum ga manyan firistoci da malaman dokoki. Za su yi masa hukuncin kisa 19 za
su kuma bashe shi ga Al’ummai su yi masa ba’a, su yi masa bulala, su kuma gicciye
shi. A rana ta uku kuma a tashe shi!”

### *Roƙon mahaifiya*
### *(Markus 10.35-45)*

20 Sai mahaifiyar ’ya’yan Zebedin nan ta zo wurin Yesu tare da ’ya’yanta, da ta
durƙusa a ƙasa, sai ta roƙe shi yǎ yi mata wani abu.

21 Ya yi tambaya ya ce, “Mene ne kike so?”

Ta ce, “Ka sa daga cikin ’ya’yan nan nawa biyu, ɗaya yǎ zauna a damarka, ɗaya
kuma a hagunka, a mulkinka.”

22 Yesu ya ce musu, “Ba ku san abin da kuke roƙo ba. Za ku iya sha daga kwaf da
zan sha?”
Suka amsa, “Za mu iya.”
23 Yesu ya ce musu, “Tabbatacce za ku sha daga kwaf na, sai dai zama a damana,
ko haguna, ba ni nake da izinin bayarwa ba. Waɗannan wurare na waɗanda Ubana
ya shirya wa ne.”
24 Da goman suka ji haka, sai suka yi fushi da ’yan’uwan nan biyu. 25 Yesu ya kira
su wuri ɗaya ya ce, “Kun san cewa masu mulkin Al’ummai sukan nuna musu iko,
hakimansu kuma sukan gasa musu iko. 26 Ba haka zai kasance da ku ba. Maimakon
haka, duk mai son zama babba a cikinku, dole yă zama bawanku, 27 kuma duk mai
son zama shugaba, dole yă zama bawanku, 28 kamar yadda Ɗan Mutum bai zo don
a bauta masa ba, sai dai don yă yi bauta, yă kuma ba da ransa fansa saboda mutane
da yawa.”

### *Makafi biyu sun sami ganin gari*
### *(Markus 10.46-52; Luka 18.35-43)*

29 Sa’ad da Yesu da almajiransa suke barin Yeriko, sai wani babban taro ya bi shi.
30 Makafi biyu kuwa suna zaune a bakin hanya, da suka ji cewa Yesu yana wucewa,
sai suka ɗaga murya suka ce, “Ubangiji, Ɗan Dawuda, ka ji tausayinmu!”
31 Mutane suka tsawata musu, suka ce musu su yi shiru. Sai suka ƙara ɗaga murya
suna cewa, “Ubangiji, Ɗan Dawuda, ka ji tausayinmu!”
32 Yesu ya tsaya ya kira su. Ya tambaye su, “Me kuke so in yi muku?”
33 Suka amsa suka ce, “Ubangiji, muna so mu sami ganin gari.”
34 Sai Yesu ya ji tausayinsu, ya taɓa idanunsu. Nan da nan kuwa suka sami ganin
gari, suka kuma bi shi.

# 21

### *Shigar mai nasara*
### *(Markus 11.1-11; Luka 19.28-38; Yohanna 12.12-19)*

1 Da suka yi kusa da Urushalima suka kuma kai Betfaji da yake kan Dutsen Zaitun,
sai Yesu ya aiki almajirai biyu, 2 yana ce musu, “Ku je ƙauyen da yake gabanku, nan
take za ku ga wata jaka a daure tare da ɗanta kusa da ita, a can. Ku kunce su ku
kawo mini. 3 In wani ya yi muku wata magana, ku ce masa Ubangiji yana bukatarsu,
zai kuwa mai da su nan da nan.”
4 Wannan ya faru ne don a cika abin da aka faɗa ta bakin annabin cewa,
5 “Ku ce wa Diyar Sihiyona,
‘Duba, sarkinki yana zuwa gare ki,
mai tawali’u yana a kan jaki,
a kan aholaki, ɗan jaki.’ ”*
6 Almajiran suka tafi suka yi kamar yadda Yesu ya umarce su. 7 Suka kawo jakar
da ɗanta, suka shimfiɗa mayafansu a kansu, Yesu kuma ya zauna a kansu. 8 Wani
babban taron mutane suka shimfiɗa mayafansu a kan hanya, yayinda waɗansu suka
sassari rassan itatuwa suka shisshimfiɗa a kan hanya. 9 Taron mutanen da suke
gabansa da kuma waɗanda suke binsa a baya suka yi ihu suna cewa,
“Hosanna† ga Ɗan Dawuda!”

“Mai albarka ne wanda yake zuwa cikin sunan Ubangiji!”‡

“Hosanna a cikin sama!”

---

* **21:5** Zak 9.9 † **21:9** Wani faɗi na Ibraniyanci mai ma’anar “Ceto!” Wanda ya kasance wani salon yabo; haka kuma a aya 15 ‡ **21:9** Zab 118.26

10 Sa'ad da Yesu ya shiga Urushalima, dukan birnin ya ruɗe, ana ta tambaya, "Wane ne wannan?"
11 Taron mutane suka amsa, "Wannan shi ne Yesu, annabin nan daga Nazaret a Galili."

### *Yesu a haikali*
### *(Markus 11.15-19; Luka 19.45-48; Yohanna 2.13-22)*

12 Yesu ya shiga filin haikali, ya kuma kori duk masu saya da sayarwa a can. Ya
tutture tebur masu canjin kuɗi da kuma kujerun masu sayar da tattabarai. 13 Ya ce
musu, "A rubuce yake, 'Za a ce da gidana, gidan addu'a,'§amma kuna mai da shi
'kogon 'yan fashi.' "*
14 Makafi da guragu suka zo wurinsa a haikali, ya kuwa warkar da su. 15 Amma
da manyan firistoci da malaman dokoki suka ga abubuwan banmamakin da ya yi,
yara kuma suna ihu a filin haikali suna cewa, "Hosanna ga Ɗan Dawuda," sai fushi
ya kama su.
16 Suka tambaye shi suka ce, "Kana jin abin da waɗannan suke faɗa?"
Yesu ya amsa ya ce, "I, ba ku taɓa karanta ba cewa,
" 'Daga leɓunan yara da jarirai
kai, Ubangiji, ka shirya wa kanka yabo'?"†
17 Sai ya bar su, ya fita daga birnin ya tafi Betani, inda ya kwana.

### *Itacen ɓaure ya yanƙwane*
### *(Markus 11.12-14,20-24)*

18 Kashegari da sassafe, yayinda yake kan hanyarsa ta komawa cikin birni, sai ya ji
yunwa. 19 Ganin itacen ɓaure kusa da hanya, sai ya je wajensa amma bai sami kome
a kansa ba sai ganye. Sai ya ce masa, "Kada ka ƙara yin 'ya'ya!" Nan da nan itacen
ya yanƙwane.
20 Sa'ad da almajiran suka ga haka, sai suka yi mamaki suna tambaya, "Yaya itacen
ɓauren ya yanƙwane nan da nan haka?"
21 Yesu ya amsa ya ce, "Gaskiya nake gaya muku, in kuna da bangaskiya, ba kuwa
da wata shakka ba, ba kawai za ku iya yin abin da aka yi wa itacen ɓauren nan ba,
amma za ku ma iya ce wa dutsen nan, 'Je ka, ka jefa kanka cikin teku,' sai yǎ faru.
22 In kun gaskata, za ku karɓi duk abin da kuka roƙa a cikin addu'a."

### *An tuhumi ikon Yesu*

23 Sai Yesu ya shiga filin haikali, yayinda yake koyarwa, sai manyan firistoci da
dattawan mutane suka zo wurinsa suka yi tambaya, "Da wane iko kake yin waɗannan
abubuwa? Kuma wa ya ba ka wannan iko?"
24 Yesu ya amsa ya ce, "Ni ma zan yi muku tambaya guda. In kuka ba ni amsa,
ni ma zan gaya muku ko da wane iko nake yin waɗannan abubuwa. 25 Baftismar
Yohanna, daga ina ta fito? Daga sama ce, ko daga mutane?"
Sai suka tattauna a junansu suka ce, "In muka ce, 'Daga sama,' zai ce, 'To, me ya
sa ba mu gaskata shi ba?' 26 In kuma muka ce, 'Daga mutane,' muna tsoron mutane,
gama duk sun ɗauka Yohanna annabi ne."
27 Saboda haka suka amsa wa Yesu suka ce, "Ba mu sani ba."
Sai ya ce, "Ni ma ba zan gaya muku ko da wane iko nake yin waɗannan abubuwa
ba."

### *Misalin 'ya'ya biyu maza*

28 "Me kuka gani? An yi wani mutum wanda yake da 'ya'ya biyu maza. Sai ya je
wajen ɗan farin ya ce, 'Ɗana, yau tafi gonar inabi ka yi aiki.'
29 "Ya amsa ya ce, 'Ba zan tafi ba,' amma daga baya ya sāke tunani, ya tafi.

§ **21:13** Ish 56.7 * **21:13** Irm 7.11 † **21:16** Zab 8.2

30 “Sai mahaifin ya tafi waje na biyun ya faɗa masa iri magana guda. Sai ya amsa
ya ce, ‘Zan tafi, ranka yă daɗe,’ amma bai tafi ba.
31 “Wanne cikin yaran nan biyu ya yi abin da mahaifinsa yake so?”
Suka amsa, “Na farin.”
Yesu ya ce musu, “Gaskiya nake gaya muku, masu karɓar haraji da karuwai suna
riga ku shiga mulkin Allah. 32 Gama Yohanna Mai Baftisma ya zo wurinku don yă
nuna muku hanyar adalci, ba ku gaskata shi ba, amma masu karɓar haraji da karuwai
sun gaskata. Har ma bayan kun ga wannan, ba ku tuba kun gaskata shi ba.”

*Misalin ’yan haya*
*(Markus 12.1-12; Luka 20.9-19)*

33 “Ku saurari wani misali. An yi wani mai gona wanda ya yi gonar inabi. Ya
kewaye ta da katanga, ya haƙa wurin matsin inabi a ciki, ya kuma gina hasumiyar
gadi. Sa’an nan ya ba wa waɗansu manoma hayar gonar inabin, ya kuma yi tafiya.
34 Da lokacin girbi ya yi kusa, sai ya aiki bayinsa wajen ’yan hayan, su karɓo masa
’ya’yan inabi.
35 “Amma ’yan hayan suka kama bayinsa; suka dūke ɗaya, suka kashe ɗaya, suka
kuma jajjefi na ukun. 36 Sai ya sāke aiken waɗansu bayi wurinsu, fiye da na dā yawa,
amma ’yan hayan suka yi musu kamar yadda suka yi wa na farin. 37 A ƙarshe, sai
ya aiki ɗansa a wurinsu. Ya ce, ‘Za su girmama ɗana.’
38 “Amma da ’yan hayan suka hangi ɗan, sai suka ce wa juna, ‘Wannan shi ne
magājin. Ku zo, mu kashe shi, mu ci gādonsa.’ 39 Saboda haka suka kama shi, suka
jefar da shi bayan katangar gonar inabin, suka kashe shi.
40 “To, idan mai gonar inabin ya zo, me zai yi da ’yan hayan nan?”
41 Suka amsa suka ce, “Zai yi wa banzan mutanen nan mugun kisa, yă ba da hayar
gonar inabin ga waɗansu ’yan haya, waɗanda za su ba shi rabonsa na amfanin gona
a lokacin girbi.”
42 Yesu ya ce musu, “Ashe, ba ku taɓa karanta a cikin Nassi cewa,
“ ‘Dutsen da magina suka ƙi shi
ne ya zama dutsen kusurwar gini.
Ubangiji ne ya aikata wannan,
kuma abin mamaki ne a idanunmu’?‡
43 “Saboda haka, ina gaya muku cewa za a karɓe mulkin Allah daga gare ku, a ba
wa mutanen da za su ba da amfani. 44 Duk wanda ya fāɗi a kan dutsen nan, zai
kakkarye. Amma duk wanda dutsen nan ya fāɗi a kansa, za a murƙushe shi.”§
45 Da manyan firistoci da Farisiyawa suka ji misalan Yesu, sai suka gane cewa da
su yake. 46 Suka nemi hanyar kama shi, amma suka ji tsoron taron, don mutane sun
ɗauka shi annabi ne.

# 22

*Misalin bikin aure*
*(Luka 14.15-24)*

1 Yesu ya sāke yin musu magana da misalai, yana cewa, 2 “Mulkin sama yana kama
da wani sarki wanda ya shirya bikin auren ɗansa. 3 Sai ya aiki bayinsa su kira
waɗanda aka gayyata zuwa bikin, amma waɗanda aka ce su zo bikin, suka ƙi zuwa.
4 “Sai ya sāke aiken waɗansu bayi ya ce, ‘Ku ce wa waɗanda aka gayyata cewa na
shirya abinci. An yanka bijimai da shanun da aka yi kiwo, kome a shirye yake. Ku
zo bikin auren mana.’

‡ **21:42** Zab 118.22,23 § **21:44** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā ba su da aya 44.

5 “Amma ba su kula ba, suka kama gabansu, ɗaya ya tafi gonarsa, ɗaya kuma ya
tafi kasuwancinsa. 6 Sauran suka kama bayinsa suka wulaƙanta su, suka kuma kashe
su. 7 Sai sarkin ya yi fushi. Ya aiki mayaƙansa suka karkashe masu kisankan nan,
aka kuma ƙone birninsu.
8 “Sa’an nan ya ce wa bayinsa, ‘Bikin aure fa ya shiryu, sai dai mutanen da na
gayyata ba su dace ba. 9 Ku bi titi-titi ku gayyato duk waɗanda kuka gani, su zo
bikin.’ 10 Saboda haka bayin suka bi titi-titi, suka tattaro duk mutanen da suka samu,
masu kirki da marasa kirki, zauren bikin ya cika makil da baƙi.
11 “Amma da sarkin ya shigo don yă ga baƙin, sai ya ga wani can da ba ya sanye
da kayan auren. 12 Ya yi tambaya ya ce, ‘Aboki, yaya ka shigo nan ba tare da rigar
aure ba?’ Mutumin ya rasa ta cewa.
13 “Sai sarkin ya ce wa fadawa, ‘Ku daure shi hannu da ƙafa, ku jefar da shi waje,
cikin duhu, inda za a yi kuka da cizon haƙora.’
14 “Gama kirayayu da yawa, amma zaɓaɓɓu kaɗan ne zaɓaɓɓu.”

*Biyan haraji ga Kaisar*
*(Markus 12.13-17; Luka 20.20-26)*

15 Sai Farisiyawa suka yi waje, suka ƙulla yadda za su yi masa tarko cikin
maganarsa. 16 Suka aiki almajiransu tare da mutanen Hiridus wurinsa. Suka ce,
“Malam, mun san kai mutum ne mai mutunci, kuma kana koyar da maganar Allah
bisa gaskiya. Mutane ba sa ɗaukan hankalinka, domin ba ka kula ko su wane ne ba.
17 To, ka gaya mana, a ra’ayinka? Ya dace a biya Kaisar haraji ko a’a?”
18 Amma Yesu da yake ya san mugun nufinsu, sai ya ce, “Ku munafukai, don me
kuke ƙoƙarin sa mini tarko? 19 Ku nuna mini kuɗin da ake biyan haraji da shi.” Sai
suka kawo masa dinari, 20 sai ya tambaye su ya ce, “Hoton wane ne wannan? Kuma
rubutun wane ne?”
21 Suka amsa, “Na Kaisar ne.”
Sai ya ce musu, “Ku ba wa Kaisar abin da yake na Kaisar, ku kuma ba wa Allah
abin da yake na Allah.”
22 Da suka ji haka, sai suka yi mamaki. Saboda haka suka ƙyale shi, suka yi
tafiyarsu.

*Aure a tashin matattu*
*(Markus 12.18-27; Luka 20.27-40)*

23 A ranan nan Sadukiyawa, waɗanda suke cewa babu tashin matattu, suka zo
wurinsa da tambaya. 24 Suka ce “Malam, Musa ya faɗa mana cewa in mutum ya mutu
ba shi da ’ya’ya, dole ɗan’uwansa yă auri gwauruwar yă kuma haifar wa ɗan’uwan
’ya’ya. 25 A cikinmu an yi ’yan’uwa guda bakwai. Na fari ya yi aure, ya mutu, da yake
bai sami ’ya’ya ba, sai ya bar matarsa wa ɗan’uwansa. 26 Haka ya faru da ɗan’uwa
na biyu da na uku, har zuwa na bakwai. 27 A ƙarshe, macen ta mutu. 28 To, a tashin
matattu, matar wa a cikinsu bakwai ɗin nan za tă zama, da yake dukansu sun aure
ta?”
29 Yesu ya amsa ya ce, “Kun ɓata, domin ba ku san Nassi ko ikon Allah ba. 30 Ai,
a tashin matattu, mutane ba za su yi aure ko su ba da aure ba; za su zama kamar
mala’iku a sama. 31 Amma game da tashi daga matattu na waɗanda suka mutu ba ku
karanta abin da Allah ya ce muku ba ne, 32 ‘Ni ne Allah na Ibrahim, Allah na Ishaku
da kuma Allah na Yaƙub’*? Ai, shi ba Allah na matattu ba ne, shi Allah na masu rai
ne.”
33 Da taro suka ji haka, sai suka yi mamakin koyarwarsa.

*Doka mafi girma*
*(Markus 12.28-34; Luka 10.25-28)*

* **22:32** Fit 3.6

34 Da jin Yesu ya ƙure Sadukiyawa, sai Farisiyawa suka tattaru. 35 Ɗaya daga
cikinsu, wani masanin Doka, ya gwada shi da wannan tambaya. 36 “Malam, wace
doka ce mafi girma a cikin dokoki?”
37 Yesu ya amsa ya ce, “ ‘Ka ƙaunaci Ubangiji Allahnka da dukan zuciyarka da
dukan ranka da kuma dukan hankalinka.’† 38 Wannan, ita ce doka ta fari da kuma
mafi girma. 39 Ta biye kuma kamar ta farkon take. ‘Ka ƙaunaci maƙwabcinka kamar
kanka.’‡ 40 Dukan Doka da Annabawa suna rataya ne a kan waɗannan dokoki biyu.”

### *Kiristi, ɗan wane ne?*
*(Markus 12.35-37; Luka 20.41-44)*

41 Yayinda Farisiyawa suke a tattare wuri ɗaya, sai Yesu ya tambaye su, 42 “Me kuke
tsammani game da Kiristi? Ɗan wane ne shi?”
Suka amsa suka ce, “Dan Dawuda.”
43 Ya ce musu, “To, ta yaya Dawuda ya yi magana ta wurin Ruhu Mai Tsarki, ya
kira shi ‘Ubangiji’? Gama ya ce,
44 “ ‘Ubangiji ya ce wa Ubangijina,
“Zauna a hannun damana,
sai na sa abokan gābanka
su zama matashin sawunka.” ’§
45 To, in Dawuda ya kira shi ‘Ubangiji,’ yaya zai zama ɗansa?” 46 Ba wanda ya iya
tanka masa, daga wannan rana kuwa ba wanda ya sāke yin karambanin yin masa
wata tambaya.

# 23

### *La’anu bakwai*
*(Markus 12.38-40; Luka 11.37-52; 20.45-47)*

1 Sa’an nan Yesu ya ce wa taron mutane da kuma almajiransa, 2 “Malaman dokoki
da Farisiyawa suke zama a kujerar Musa. 3 Saboda haka dole ku yi musu biyayya, ku
kuma yi duk abin da suka faɗa muku. Sai dai kada ku yi abin da suke yi, gama ba sa
yin abin da suke wa’azi. 4 Sukan ɗaura kaya masu nauyi, su sa wa mutane a kafaɗa.
Amma su kansu, ba sa ko sa yatsa su taimaka.
5 “Kome suke yi, suna yi ne don mutane su gani. Sukan yi layunsu*fantam-fantam
bakin rigunarsu kuma sukan kai har ƙasa; 6 suna son wurin zaman manya a wurin
biki, da kuma wuraren zama gaba-gaba a majami’u; 7 suna so a yi ta gaisuwarsu a
kasuwa, ana kuma riƙa ce musu, ‘Rabbi.’
8 “Amma kada a kira ku ‘Rabbi,’ gama kuna da Maigida ɗaya ne, ku duka kuwa,
’yan’uwa ne. 9 Kada kuma ku kira wani a duniya ‘uba,’ gama kuna da Uba ɗaya
ne, yana kuwa a sama. 10 Ba kuwa za a kira ku ‘malam’ ba, gama kuna da Malami
ɗaya ne, Kiristi. 11 Mafi girma a cikinku, zai zama bawanku. 12 Gama duk wanda ya
ɗaukaka kansa, za a ƙasƙantar da shi, duk kuma wanda ya ƙasƙantar da kansa, za
a ɗaukaka shi.
13 “Kaitonku, malaman dokoki da Farisiyawa, ku munafukai! Kun rufe ƙofar
mulkin sama a gaban mutane. Ku kanku ba ku shiga ba, ba kuwa bar waɗanda
suke ƙoƙarin shiga su shiga ba.†
15 “Kaitonku, malaman dokoki da Farisiyawa, munafukai! Kukan yi tafiye-tafiye
zuwa ƙasashe, ku ƙetare teku don ku sami mai tuba ɗaya, sa’ad da ya tuba kuwa,
sai ku mai da shi ɗan wuta fiye da ku, har sau biyu.

† **22:37** M Sh 6.5 ‡ **22:39** Fir 19.18 § **22:44** Zab 110.1 * **23:5** Wato, akwatuna ƙunshe da ayoyin Maganar Allah, daure a goshinsu da kuma a hannuwansu † **23:13** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da zuwa. 14 Kaitonku, malaman dokoki da Farisiyawa, ku munafukai! Kukan ci kayan gidan matan da mazansu suka mutu, kukan yi doguwar addu’a don ɓad da sawu. Saboda haka za a yi muku hukunci mafi tsanani.

[16] “Kaitonku, makafi jagora! Kukan ce, ‘In wani ya rantse da haikali, ba damuwa;
amma in ya rantse da zinariyar haikali, sai rantsuwar ta kama shi.’ [17] Wawaye
makafi! Wanne ya fi girma, zinariyar, ko haikalin da yake tsarkake zinariyar?
[18] Kukan kuma ce, ‘In wani ya rantse da bagade, ba damuwa; amma in ya rantse
da bayarwar da take bisansa, sai rantsuwar ta kama shi.’ [19] Makafi kawai! Wanne ya
fi girma, bayarwar, ko kuwa bagaden da yake tsarkake bayarwar? [20] Saboda haka,
duk wanda ya rantse da bagade, ya rantse ne da bagaden tare da abin da yake bisansa.
[21] Kuma duk wanda ya rantse da haikali, ya rantse ne da shi da kuma wanda yake
zaune a cikinsa. [22] Duk kuma wanda ya rantse da sama, ya rantse ne da kursiyin
Allah da kuma wanda yake zaune a kansa.
[23] “Kaitonku, malaman dokoki da Farisiyawa, munafukai! Kukan ba da kashi ɗaya
bisa goma na kayan yajinku, naʼanaʼa, anise, da lafsur. Amma kun ƙyale abubuwan
da suka fi girma na dokoki, adalci, jinƙai da aminci. Waɗannan ne ya kamata da
kun kiyaye ba tare da kun ƙyale sauran ba. [24] Makafi jagora! Kukan tace ƙwaro ɗan
mitsil amma sai ku haɗiye raƙumi.
[25] “Kaitonku, malaman dokoki da Farisiyawa, munafukai! Kukan wanke bayan
kwaf da kwano, amma a ciki, cike suke da zalunci da sonkai. [26] Kai makaho
Bafarisiye! Ka fara wanke cikin kwaf da kwano, saʼan nan bayan ma zai zama da
tsabta.
[27] “Kaitonku, malaman dokoki da Farisiyawa, munafukai! Kuna kama da
kaburburan da aka shafa musu farin fenti, waɗanda suna da kyan gani a waje, amma
a ciki, cike suke da ƙasusuwan matattu da kuma kowane irin abu mai ƙazanta.
[28] Haka ku ma, a waje, a idon mutane, ku masu adalci ne, amma a ciki, cike kuke da
munafunci da mugunta.
[29] “Kaitonku, malaman dokoki da Farisiyawa, munafukai! Kukan gina kaburbura
don annabawa, ku kuma yi wa kaburburan mutane masu adalci ado. [30] Kuna cewa,
‘Da mun kasance a zamanin kakanninmu, ai, da ba mu haɗa hannu da su muka
karkashe annabawa ba.’ [31] Ta haka kuna ba da shaida a kanku cewa ku zuriyar
waɗanda suka karkashe annabawa ne. [32] To, sai ku ci gaba ku cikasa ayyukan da
kakanninku suka fara!
[33] “Ku macizai! ʼYaʼyan macizai! Ta yaya za ku tsere wa hukuncin jahannama ta
wuta? [34] Saboda haka ina aika muku da annabawa, da masu hikima da malamai.
Waɗansunsu za ku kashe ku kuma gicciye; waɗansu kuma za ku yi musu bulala
a majamiʼunku kuna kuma binsu gari-gari. [35] Ta haka alhakin jinin masu adalcin
da aka zubar a duniya, tun daga jinin Habila mai adalci, zuwa jinin Zakariya ɗan
Berekiya, wanda kuka kashe tsakanin haikali da bagade zai koma kanku. [36] Gaskiya
nake gaya muku, duk wannan zai auko wa wannan zamani.

*(Luka 13.34,35)*

[37] “Urushalima, ayya Urushalima, ke da kike kashe annabawa, kike kuma jifan
waɗanda aka aiko gare ki, sau da sau na so in tattara ʼyaʼyanki wuri ɗaya, yadda
kaza takan tattara ʼyaʼyanta cikin fikafikanta, amma kuka ƙi. [38] Ga shi, an bar muku
gidanku a yashe. [39] Gama ina gaya muku, ba za ku sāke ganina ba sai kun ce, ‘Mai
albarka ne wanda yake zuwa cikin sunan Ubangiji.’ ”‡

# 24

*Alamun ƙarshen zamani*
*(Markus 13.1,2; Luka 21.5,6)*

[1] Yesu ya bar haikali ke nan, yana cikin tafiya sai almajiransa suka zo wurinsa
don su ja hankalinsa ga gine-ginen haikali. [2] Sai Yesu ya ce, “Kun ga duk waɗannan

‡ **23:39** Zab 118.26

abubuwa? Gaskiya nake gaya muku, ba wani dutse a nan da za a bari a kan wani;
duk za a rushe.”

*(Markus 13.3-13; Luka 21.7-19)*

3 Da Yesu yana zaune a Dutsen Zaitun, almajiran suka zo wurinsa a ɓoye. Suka
ce, “Gaya mana, yaushe ne wannan zai faru, mece ce alamar zuwanka da kuma ta
ƙarshen zamani?”

4 Yesu ya amsa, “Ku lura fa, kada wani yă ruɗe ku. 5 Gama mutane da yawa za su
zo cikin sunana, suna cewa, ‘Ni ne Kiristi,’ za su kuwa ruɗi mutane da yawa. 6 Za ku
ji labarin yaƙe-yaƙe da kuma jita-jitarsu, sai dai ku lura kada hankalinku yă tashi.
Dole irin waɗannan abubuwa su faru, amma ƙarshen tukuna. 7 Al’umma za tă tasar
wa al’umma, mulki yă tasar wa mulki. Za a yi yunwa da girgizar ƙasa a wurare
dabam-dabam. 8 Dukan waɗannan fa, mafarin azabar naƙudar haihuwa ne.

9 “Sa’an nan za a bashe ku don a tsananta muku a kuma kashe ku, dukan al’ummai
za su ƙi ku saboda ni. 10 A wannan lokaci, da yawa za su juya daga bangaskiya,
su ci amana su kuma ƙi juna, 11 annabawan ƙarya da yawa za su firfito su kuma
ruɗi mutane da yawa. 12 Saboda ƙaruwar mugunta, ƙaunar yawanci za tă yi sanyi,
13 amma duk wanda ya tsaya da ƙarfi har ƙarshe, zai sami ceto. 14 Za a kuma yi
wa’azin wannan bisharar mulki a cikin dukan duniya, yă zama shaida ga dukan
al’ummai, sa’an nan ƙarshen yă zo.

*(Markus 13.14-23; Luka 21.20-24)*

15 “Saboda haka sa’ad da kuka ga ‘abin ƙyama mai kawo hallaka,’*wanda annabi
Daniyel ya yi magana a kai, yana tsaye a tsattsarkan wuri (mai karatu yă gane), 16 to,
sai waɗanda suke cikin Yahudiya, su gudu zuwa cikin duwatsu. 17 Kada wani da yake
a kan rufin gidansa, yă sauko don ɗaukar wani abu a gida. 18 Kada wani da yake gona
kuma yă komo don ɗaukar rigarsa. 19 Kaiton mata masu ciki da mata masu renon
’ya’ya a waɗancan kwanakin! 20 Ku yi addu’a, kada gudunku yă zama a lokacin sanyi
ko a ranar Asabbaci. 21 Gama a lokacin za a yi wata matsananciyar wahala, wadda
ba a taɓa yi ba tun farkon duniya har ya zuwa yanzu ba kuwa za a ƙara yi ba.

22 “Da ba don an taƙaita kwanakin nan ba, da babu wani da zai tsira, amma saboda
zaɓaɓɓun nan, za a taƙaita kwanakin. 23 A lokacin in wani ya ce muku, ‘Duba,
ga Kiristi nan!’ Ko, ‘Ga shi can!’ Kada ku gaskata. 24 Gama Kiristi masu yawa na
ƙarya, da annabawan ƙarya za su firfito, su kuma aikata manyan alamu da ayyukan
banmamaki don su ruɗi har da zaɓaɓɓu ma in zai yiwu. 25 Ga shi, na faɗa muku tun
da wuri.

26 “Saboda haka in wani ya ce muku, ‘Ga shi can a hamada,’ kada ku fita; ko, ‘Ga shi
nan a ɗakunan ciki,’ kada ku gaskata. 27 Gama kamar yadda walƙiya take wulgawa
walai daga gabas zuwa yamma, haka dawowar Ɗan Mutum zai kasance. 28 Duk inda
mushe yake, can ungulai za su taru.

*(Markus 13.24-27; Luka 21.25-28)*

29 “Nan da nan bayan tsabar wahalan nan

“ ‘sai a duhunta rana,
wata kuma ba zai ba da haskensa ba;
taurari kuma za su fāffāɗi daga sararin sama,
za a kuma girgiza abubuwan sararin sama.’†

30 “A sa’an nan ne alamar dawowar Ɗan Mutum zai bayyana a sararin sama, dukan
al’umman duniya kuwa za su yi kuka. Za su ga Ɗan Mutum yana zuwa kan gizagizan
sararin sama, da iko da kuma ɗaukaka mai girma. 31 Zai kuwa aiki mala’ikunsa su

* **24:15** Dan 9.27; Dan 11.31; Dan 12.11 † **24:29** Ish 13.10; Ish 34.4

busa ƙaho mai ƙara sosai, za su kuwa tattaro zaɓaɓɓunsa daga kusurwoyi huɗun
nan, daga wannan bangon duniya zuwa wancan.

*(Markus 13.28-31; Luka 21.29-33)*

32 “Yanzu fa, sai ku koyi wannan darasi daga itacen ɓaure. Da zarar rassansa suka
yi taushi ganyayensa kuma suka toho, kun san damina ta kusa. 33 Haka kuma, sa’ad
da kun ga dukan waɗannan abubuwa, ku sani ya yi kusan zuwa, yana ma dab da
bakin ƙofa. 34 Gaskiya nake gaya muku, wannan zamani ba zai shuɗe ba sai dukan
abubuwan nan sun faru. 35 Sama da ƙasa za su shuɗe, amma maganata ba za tă taɓa
shuɗe ba.

*Rana ko sa’a ba a sani ba*
*(Markus 13.32-37; Luka 17.26-30,34-35)*

36 “Babu wanda ya san wannan rana ko sa’a, ko mala’ikun da suke sama ma, ko
Ɗan, sai dai Uban kaɗai. 37 Kamar yadda ya faru a zamanin Nuhu, haka zai zama
a dawowar Ɗan Mutum. 38 Gama a kwanaki kafin ruwan tsufana, mutane sun yi ta
ci, sun kuma yi ta sha, suna aure, suna kuma aurarwa, har zuwa ranar da Nuhu ya
shiga jirgi; 39 ba su kuwa san abin da yake faruwa ba sai da ruwan tsufana ya zo ya
share su tas. Haka zai zama a dawowar Ɗan Mutum. 40 Maza biyu za su kasance a
gona; za a ɗau ɗaya a bar ɗaya. 41 Mata biyu za su kasance suna niƙa; za a ɗau ɗaya
a bar ɗaya.

42 “Saboda haka sai ku zauna a faɗake, gama ba ku san a wace rana ce Ubangijinku
zai zo ba. 43 Ku dai gane wannan, da maigida ya san ko a wane lokaci ne da dare,
ɓarawo zai zo, da sai yă zauna a faɗake yă kuma hana a shiga masa gida. 44 Saboda
haka ku ma, sai ku zauna a faɗake, domin Ɗan Mutum zai zo a sa’ar da ba ku za tă
ba.

*(Luka 12.35-48)*

45 “Wane ne bawan nan mai aminci da kuma mai hikima, wanda maigida ya sa
yă lura da bayi a cikin gidansa, yă riƙa ba su abinci a daidai lokaci? 46 Zai zama
wa bawan nan da kyau in maigidan ya dawo ya same shi yana yin haka. 47 Gaskiya
nake gaya muku, zai sa shi yă lura da dukan dukiyarsa. 48 Amma in wannan bawa
mugu ne, ya kuma ce a ransa, ‘Maigidana ba zai dawo da wuri ba.’ 49 Sa’an nan yă
fara dūkan ’yan’uwansa bayi, yana ci yana kuma sha tare da mashaya. 50 Maigidan
wannan bawa zai dawo a ranar da bai yi tsammani ba, a sa’ar kuma da bai sani ba.
51 Maigidan zai farfasa masa jiki da bulala, yă kuma ba shi wuri tare da munafukai,
inda za a yi kuka da cizon haƙora.

## 25

*Misalin budurwai goma*

1 “A lokacin mulkin sama zai zama kamar budurwai goma waɗanda suka ɗauki
fitilunsu suka fita don su taryi ango. 2 Biyar daga cikinsu wawaye ne, biyar kuma
masu hikima. 3 Wawayen sun ɗauki fitilunsu, sai dai ba su riƙe mai ba. 4 Masu
hikimar kuwa suka riƙo tulunan mai da fitilunsu. 5 Ango ya yi jinkirin zuwa, sai duk
suka shiga gyangyaɗi har barci ya kwashe su.

6 “Can tsakar dare, sai aka ji kira, ana cewa, ‘Ga ango nan! Ku fito, ku tarye shi!’

7 “Sai dukan budurwan nan suka farka suka kuna fitilunsu. 8 Sai wawayen suka ce
wa masu hikimar, ‘Ku ɗan sassam mana manku; fitilunmu suna mutuwa.’

9 “Su kuwa suka amsa, suka ce, ‘A’a, wataƙila ba zai ishe mu da ku ba. Gara ku je
wurin masu sayarwa ku sayo.’

10 “Amma yayinda suke kan tafiya garin sayen mai, sai ango ya iso. Budurwai da
suke a shirye, suka shiga wajen bikin auren tare da shi. Aka kuma kulle ƙofa.

11 “An jima can, sai ga sauran sun iso. Suka ce, ‘Ranka yă daɗe! Ranka yă daɗe!
Ka buɗe mana ƙofa!’
12 “Amma ya amsa ya ce, ‘Gaskiya nake gaya muku, ban san ku ba.’
13 “Saboda haka sai ku zauna a faɗake, don ba ku san ranar ko sa’ar ba.

*Misalin talenti*
*(Luka 19.11-27)*

14 “Har wa yau, za a kwatanta shi da mutumin da zai yi tafiya, wanda ya kira
bayinsa ya kuma danƙa musu mallakarsa. 15 Ga guda, ya ba shi talenti biyar na
kuɗi, ga wani talenti biyu, ga wani kuma talenti ɗaya, kowa bisa ga azancinsa. Sa’an
nan ya yi tafiyarsa. 16 Mutumin da ya karɓi talenti biyar, nan da nan ya tafi ya yi
kasuwanci da su har ya sami ribar talenti biyar. 17 Haka ma, wannan mai talenti
biyu, shi ma ya yi riba biyu. 18 Amma mutumin da ya karɓi talenti ɗaya ɗin, ya tafi,
ya tona rami, ya ɓoye kuɗin maigidansa.
19 “Bayan an daɗe, sai maigidan bayin nan ya dawo, ya kuma daidaita lissafi da su.
20 Mutumin da ya karɓi talenti biyar, ya kawo ƙarin talenti biyar. Ya ce, ‘Maigida, ka
danƙa mini talenti biyar. Ga shi, na yi ribar biyar.’
21 “Maigidansa ya amsa ya ce, ‘Madalla, bawan kirki mai aminci! Ka yi aminci a
kan abubuwa kaɗan, zan sa ka lura da abubuwa masu yawa. Zo ka yi farin ciki tare
da maigidanka!’
22 “Mutumin da yake da talenti biyu, shi ma ya zo ya ce, ‘Maigida, ka danƙa mini
talenti biyu; ga shi, na yi ribar biyu.’
23 “Maigidansa ya amsa ya ce, ‘Madalla, bawan kirki mai aminci! Ka yi aminci a
kan abubuwa kaɗan, zan sa ka lura da abubuwa masu yawa. Zo ka yi farin ciki tare
da maigidanka!’
24 “Sa’an nan mutumin da ya karɓi talenti ɗaya ya zo. Ya ce, ‘Maigida, na san cewa
kai mutum ne mai wuyan sha’ani, kana girbi inda ba ka shuka ba, kana kuma tara
inda ba ka yafa iri ba. 25 Saboda haka na ji tsoro, na je na ɓoye talentinka a ƙasa. Ga
abinka.’
26 “Maigidansa ya amsa ya ce, ‘Kai mugun bawa, mai ƙyuya! Ashe, ka san cewa
ina girbi inda ban yi shuka ba, ina kuma tarawa inda ban yafa iri ba? 27 To, in haka
ne, ai, da ka sa kuɗina a banki, don sa’ad da na dawo da na karɓi abina da riba.
28 “ ‘Karɓi talentin daga hannunsa ku ba wanda yake da talenti goma. 29 Gama
duk mai abu za a ƙara masa, zai kuma same shi a yawalce. Duk wanda ba shi da
shi kuwa, ko ɗan abin da yake da shi ma, sai an karɓe masa. 30 Ku jefar da banzan
bawan nan waje, cikin duhu, inda za a yi kuka da cizon haƙora.’

*Tumaki da awaki*

31 “Sa’ad da Ɗan Mutum ya zo cikin ɗaukakarsa, tare da dukan mala’iku, zai zauna
a kursiyinsa cikin ɗaukakar sama. 32 Za a tara dukan al’ummai a gabansa, zai kuma
raba mutane dabam-dabam yadda makiyayi yakan ware tumaki daga awaki. 33 Zai
sa tumaki a damansa, awaki kuma a hagunsa.
34 “Sa’an nan Sarki zai ce wa waɗanda suke damansa, ‘Ku zo, ku da Ubana ya yi wa
albarka; ku karɓi gādonku, mulkin da aka shirya muku tun halittar duniya. 35 Gama
da nake jin yunwa, kun ciyar da ni, da nake jin ƙishirwa, kun ba ni abin sha, da nake
baƙunci, kun karɓe ni, 36 da nake bukatar tufafi, kun yi mini sutura, da na yi rashin
lafiya, kun lura da ni, da nake kurkuku, kun ziyarce ni.’
37 “Sa’an nan masu adalci za su amsa masa, su ce, ‘Ubangiji, yaushe muka gan ka
da yunwa muka ciyar da kai, ko da ƙishirwa muka ba ka abin sha? 38 Yaushe kuma
muka gan ka baƙo muka karɓe ka, ko cikin bukatar tufafi muka yi maka sutura?
39 Yaushe kuma muka gan ka cikin rashin lafiya ko a kurkuku muka ziyarce ka?’

40 “Sarkin zai amsa ya ce, ‘Gaskiya nake gaya muku, duk abin da kuka yi wa ɗaya
daga cikin waɗannan ’yan’uwana mafi ƙanƙanta, ni kuka yi wa.’
41 “Sa’an nan zai ce wa waɗanda suke a hagunsa, ‘Ku rabu da ni, la’anannu, zuwa
cikin madawwamiyar wutar da aka shirya don Iblis da mala’ikunsa. 42 Gama da nake
jin yunwa, ba ku ba ni abinci ba, da nake jin ƙishirwa, ba ku ba ni abin sha ba, 43 da
na yi baƙunci, ba ku karɓe ni ba, da nake bukatar tufafi, ba ku yi mini sutura ba, da
na yi rashin lafiya kuma ina a kurkuku, ba ku lura da ni ba.’
44 “Su ma za su amsa, su ce, ‘Ubangiji, yaushe muka gan ka cikin yunwa ko ƙishirwa
ko baƙo ko cikin bukatar tufafi ko cikin rashin lafiya ko cikin kurkuku, ba mu taimake
ka ba?’
45 “Zai amsa, yǎ ce, ‘Gaskiya nake gaya muku, duk abin da ba ku yi wa ɗaya daga
cikin waɗannan mafi ƙanƙanta ba, ba ku yi mini ba ke nan.’
46 “Sa’an nan za su tafi cikin madawwamiyar hukunci, amma masu adalci kuwa za
su shiga rai madawwami.”

# 26

*An ƙulla shawara gāba da Yesu*
*(Markus 14.1,2; Luka 22.1,2; Yohanna 11.45-53)*

1 Sa’ad da Yesu ya gama faɗin dukan waɗannan abubuwa, sai ya ce wa almajiransa,
2 “Kamar yadda kuka sani, Bikin Ketarewa sauran kwana biyu, za a kuma ba da Ɗan
Mutum don a gicciye shi.”
3 Sai manyan firistoci da dattawan mutane, suka taru a fadan babban firist, mai
suna Kayifas, 4 suka ƙulla shawara su kama Yesu da makirci, su kuma kashe shi.
5 Suka ce, “Amma ba a lokacin Biki ba, don kada mutane su tā da rikici.”

*An shafe Yesu a Betani*
*(Markus 14.3-9; Yohanna 12.1-8)*

6 Yayinda Yesu yake a Betani, a gidan wani mutumin da ake kira Siman Kuturu,
7 wata mace ta zo wurinsa da wani ɗan tulun alabasta na turaren mai tsada sosai,
wanda ta zuba a kansa a lokacin da yake cin abinci.
8 Sa’ad da almajiransa suka ga wannan, sai suka yi fushi. Suka ce, “Wannan
almubazzaranci fa! 9 Wannan turare ai, da an sayar da shi da kuɗi mai yawa a
ba matalauta kuɗin.”
10 Sane da wannan, Yesu ya ce musu, “Me ya sa kuke damun macen nan? Ta yi
mini abu mai kyau ne. 11 Matalauta za su kasance tare da ku kullum, amma ni ba
zan kasance tare da ku kullum ba. 12 Sa’ad da ta zuba turaren nan a jikina, ta shirya
ni ne don jana’izata. 13 Gaskiya nake gaya muku, duk inda aka yi wa’azin bisharan
nan a duniya duka, abin da matan nan ta yi, za a riƙa faɗarsa don tunawa da ita.”

*Yahuda ya yarda yǎ bashe Yesu*

14 Sai ɗaya daga cikin Sha Biyun nan, wanda ake kira Yahuda Iskariyot, ya je wurin
manyan firistoci 15 ya ce, “Me za ku ba ni, in na bashe shi gare ku?” Sai suka ƙirga
masa kuɗi azurfa talatin. 16 Daga wannan lokaci, Yahuda ya yi ta neman zarafin da
zai miƙa shi.

*Abincin yamma na Ubangiji*
*(Markus 14.12-21; Luka 22.7-13; Yohanna 13.21-30)*

17 A rana ta fari ta Bikin Burodi Marar Yisti, sai almajiran suka zo wurin Yesu suka
yi tambaya suka ce, “Ina kake so mu je mu shirya maka wurin da za ka ci Bikin
Ketarewa?”

18 Ya amsa ya ce, “Ku shiga gari wurin wāne, ku ce masa, ‘Malam ya ce, lokacina
ya yi kusa. Zan ci Bikin Ketarewa tare da almajiraina a gidanka.’ ” 19 Saboda haka
almajiran suka yi yadda Yesu ya umarce su, suka kuwa shirya Bikin Ketarewa.
20 Da yamma ta yi, sai Yesu ya zauna don cin abinci tare da Sha Biyun. 21 Yayinda
suke cin abinci, sai ya ce, “Gaskiya nake gaya muku, ɗayanku zai bashe ni.”
22 Suka yi baƙin ciki ƙwarai, suka fara ce masa da ɗaya-ɗaya, “Gaskiya nake gaya
muku, ɗayanku zai bashe ni.”
23 Yesu ya amsa ya ce, “Wanda ya sa hannunsa a kwano tare da ni ne, zai bashe ni.
24 Ɗan Mutum zai tafi kamar yadda aka rubuta game da shi. Amma kaiton mutumin
da zai bashe Ɗan Mutum! Da ma ba a haifi mutumin nan ba, da ya fi masa.”
25 Sa’an nan Yahuda, wanda zai bashe shi ya ce, “Tabbatacce ba ni ba ne, ko, Rabbi?”
Yesu ya amsa ya ce, “I, kai ma ka fada.”[*]

*(Markus 14.22-26; Luka 22.14-23; 1 Korintiyawa 11.23-25)*

26 Yayinda suke cikin cin abinci, Yesu ya ɗauki burodi, ya yi godiya ya kuma
kakkarya, ya ba wa almajiransa yana cewa, “Ku karɓa ku ci; wannan jikina ne.”
27 Sa’an nan ya ɗauki kwaf, ya yi godiya, ya kuma ba su, yana cewa, “Ku shassha
daga cikinsa, dukanku. 28 Wannan jinina ne na sabon alkawari, wanda aka zubar
saboda mutane da yawa, don gafarar zunubai. 29 Ina gaya muku, ba zan ƙara shan
ruwan inabin nan ba har sai ranar da zan sha shi sabo tare da ku a mulkin Ubana.”
30 Da suka rera waƙa, sai suka fita, suka tafi Dutsen Zaitun.

## *Yesu ya yi maganar mūsun da Bitrus zai yi*
*(Markus 14.27-31; Luka 22.31-34; Yohanna 13.36-38)*

31 Sai Yesu ya ce musu, “A wannan dare, dukanku za ku ja da baya saboda ni, gama
a rubuce yake cewa,
“ ‘Zan bugi makiyayin,
tumakin garken kuwa za su fasu.’[†]
32 Amma bayan na tashi, zan sha gabanku zuwa Galili.”
33 Bitrus ya amsa ya ce, “Ko da duka sun ja da baya saboda kai, ba zan taɓa ja da
baya ba.”
34 Yesu ya amsa ya ce, “Gaskiya nake gaya maka, a daren nan, kafin zakara yǎ yi
cara, za ka yi mūsun sanina sau uku.”
35 Bitrus ya furta, “Ko da ma zan mutu ne tare da kai, ba zan taɓa yin mūsun
saninka ba.” Dukan sauran almajiran ma suka faɗa haka.

## *Getsemane*
*(Markus 14.32-42; Luka 22.39-46)*

36 Sa’an nan Yesu ya tafi da almajiransa zuwa wani wurin da ake kira Getsemane,
ya ce musu, “Ku zauna nan, in je can in yi addu’a.” 37 Ya ɗauki Bitrus da ’ya’ya biyun
nan na Zebedi tare da shi, sai ya fara baƙin ciki, ya kuma damu. 38 Sai ya ce musu,
“Raina yana cike da baƙin ciki har kamar zan mutu. Ku dakata a nan, ku kuma yi
tsaro tare da ni.”
39 Da ya yi gaba kaɗan, sai ya fāɗi a ƙasa, ya yi addu’a ya ce, “Ubana, in mai
yiwuwa ne, a ɗauke mini wannan kwaf. Amma ba nufina ba, sai naka.”
40 Sa’an nan ya komo wurin almajiransa, ya tarar suna barci. Ya tambayi Bitrus
ya ce, “Ashe, ba za ku iya yin tsaro tare da ni ko na sa’a guda ba? 41 Ku yi tsaro, ku
kuma yi addu’a, don kada ku fāɗi cikin jarraba. Ruhu yana so, sai dai jiki raunana
ne.”
42 Ya sāke tafiya sau na biyu, ya yi addu’a ya ce, “Ubana, in ba zai yiwu a ɗauke
wannan kwaf ba sai na sha shi, to, bari a aikata nufinka.”

[*] **26:25** Ko kuwa “Kai kanka ka faɗa” [†] **26:31** Zak 13.7

43 Da ya dawo, har yanzu ya tarar suna barci, domin idanunsu sun yi nauyi da
barci. 44 Saboda haka ya sāke barinsu, ya yi addu'a sau na uku, yana maimaita iri
abu guda.
45 Sa'an nan ya komo wurin almajiransa, ya ce musu, "Har yanzu kuna barci kuna
hutawa ba? Ga shi, sa'a ta yi kusa, an kuma bashe Ɗan Mutum a hannuwan masu
zunubi. 46 Ku tashi, mu tafi! Ga mai bashe ni nan yana zuwa!"

*An kama Yesu*
*(Markus 14.43-50; Luka 22.47-53; Yohanna 18.3-12)*

47 Yayinda yana cikin magana, sai Yahuda, ɗaya daga cikin Sha Biyun nan, ya iso.
Tare da shi kuwa ga taro mai yawa riƙe da takuba da sanduna, manyan firistoci da
dattawan mutane ne suka turo su. 48 To, mai bashe shi ɗin, ya riga ya shirya alama
da su, "Wanda na yi masa sumba, shi ne mutumin; ku kama shi." 49 Da zuwansa, sai
ya miƙe zuwa wurin Yesu ya ce, "Gaisuwa, Rabbi!" Sa'an nan ya yi masa sumba.
50 Yesu ya amsa ya ce, "Aboki, yi abin da ya kawo ka."‡

Sa'an nan mutanen suka matso, suka kama Yesu suka riƙe shi. 51 Ganin haka, sai
ɗaya daga cikin waɗanda suke tare da Yesu, ya zaro takobinsa ya kai wa bawan
babban firist sara, ya fille masa kunne.
52 Sai Yesu ya ce, masa, "Mai da takobinka kube, gama duk masu zare takobi, a
takobi za su mutu. 53 Kuna tsammani ba zan iya kira Ubana, nan take kuwa yǎ aiko
mini fiye da rundunar mala'iku goma sha biyu ba? 54 Amma ta yaya za a cika Nassin
da ya ce dole haka yǎ faru?"
55 A wannan lokaci sai Yesu ya ce wa taron, "Ina jagoran wani tawaye ne, da kuka
fito da takuba da kuma sanduna domin ku kama ni? Kowace rana ina zama a filin
haikali ina koyarwa, ba ku kuwa kama ni ba. 56 Amma wannan duka ya faru ne don
a cika rubuce-rubucen annabawa." Sa'an nan dukan almajiran suka yashe shi suka
gudu.

*A gaban majalisa*
*(Markus 14.53-65; Luka 22.54,55,63-71; Yohanna 18.13,14,19-24)*

57 Waɗanda suka kama Yesu kuwa suka kai shi wurin Kayifas, babban firist, inda
malaman dokoki da dattawa suka taru. 58 Amma Bitrus ya bi daga nesa, har zuwa
cikin filin gidan babban firist. Ya shiga, ya zauna tare da masu gadi, don yǎ ga
ƙarshen abin.
59 Sai manyan firistoci da 'yan majalisa duka suka yi ta neman shaidar ƙarya a kan
Yesu, don su sami dama su kashe shi. 60 Amma ba su sami ko ɗaya ba, ko da yake
masu shaidar ƙarya da yawa sun firfito.

A ƙarshe, biyu suka zo gaba, 61 suka furta cewa, "Wannan mutum ya ce, 'Ina iya
rushe haikalin Allah, in sāke gina shi cikin kwana uku.' "
62 Sa'an nan babban firist ya miƙe tsaye, ya ce wa Yesu, "Ba ka da wata amsa?
Shaidar da mutanen nan suke yi a kanka fa?" 63 Amma Yesu ya yi shiru.

Sai babban firist ya ce masa, "Na haɗa ka da Allah mai rai. Faɗa mana in kai ne
Kiristi, Ɗan Allah."
64 Sai Yesu ya amsa ya ce, "I, haka yake yadda ka faɗa. Sai dai ina gaya muku duka,
nan gaba, za ku ga Ɗan Mutum zaune a hannun dama na Mai Iko, yana kuma zuwa
a kan gizagizan sama."
65 Sa'an nan babban firist ya yage tufafinsa ya ce, "Ya yi saɓo! Don me muke
bukatar ƙarin shaidu? Ga shi, yanzu kun dai ji saɓon. 66 Me kuka gani?"

Suka amsa, suka ce, "Ya cancanci mutuwa."

‡ **26:50** Ko kuwa "Aboki, me ya kawo ka?"

67 Sai suka tottofa masa miyau a fuskarsa, suka kuma bubbuge shi da hannuwansu.
Waɗansu kuma suka mammare shi 68 suka ce, “Yi mana annabci, Kiristi. Wa ya buge
ka?”

*Bitrus ya yi mūsun sanin Yesu*
*(Markus 14.66-72; Luka 22.56-62; Yohanna 18.15-18,25-27)*

69 To, Bitrus yana nan zaune a filin, sai wata yarinya baiwa, ta zo wurinsa. Ta ce,
“Kai ma kana tare da Yesu mutumin Galili.”
70 Amma ya yi mūsu a gabansu duka. Ya ce, “Ban san abin da kike magana ba.”
71 Sa’an nan ya fito zuwa hanyar shiga, inda wata yarinya kuma ta gan shi, ta ce
wa mutanen da suke can, “Wannan mutum ma yana tare da Yesu Banazare.”
72 Ya sāke mūsu har da rantsuwa, yana cewa, “Ban ma san mutumin nan ba!”
73 Bayan ɗan lokaci, sai na tsattsaye a wurin, suka hauro wurin Bitrus, suka ce,
“Tabbatacce, kai ɗayansu ne, don harshen maganarka, ya tone ka.”
74 Sai ya fara la’antar kansa, yana ta rantsuwa yana ce musu, “Ban ma san mutumin
nan ba!”
Nan da take, sai zakara ya yi cara. 75 Sai Bitrus ya tuna da maganar da Yesu ya yi
cewa, “Kafin zakara yǎ yi cara, za ka yi mūsun sani na sau uku.” Sai ya fita waje, ya
yi ta kuka.

# 27

*Yahuda ya rataye kansa*
*(Markus 15.1; Luka 23.1,2; Yohanna 18.28-32)*

1 Da wayewar gari, sai dukan manyan firistoci da dattawan mutane suka yanke
shawara su kashe Yesu. 2 Suka daure shi, suka tafi da shi, suka ba da shi ga gwamna
Bilatus.

*(Ayyukan Manzanni 1.18,19)*

3 Sa’ad da Yahuda, wanda ya bashe Yesu, ya ga an yanke wa Yesu hukuncin kisa,
sai ya yi “da na sani.” Ya je mayar wa manyan firistoci da dattawan kuɗin azurfa
talatin ɗin. 4 Ya ce, “Na yi zunubi da na ci amanar marar laifi.”
Suka ce masa, “Ina ruwanmu da wannan? Wannan dai ruwanka ne.”
5 Sai Yahuda ya zubar da kuɗin a cikin haikalin ya tafi. Sa’an nan ya je ya rataye
kansa.
6 Manyan firistoci suka ɗauki kuɗin, suka ce, “Doka ta hana a sa kuɗin a cikin
ma’aji, da yake kuɗin jini ne.” 7 Saboda haka, sai suka yanke shawara su yi amfani
da kuɗin suka sayi filin mai yin tukwane, saboda binne baƙi. 8 Shi ya sa ake kiran
filin, Filin Jini har yǎ zuwa yau. 9 Sai abin da aka faɗa ta bakin annabi Irmiya ya
cika cewa, “Suka ɗauki azurfa talatin, kuɗin da mutanen Isra’ila suka sa a kansa,
10 suka kuma yi amfani da su, suka sayi filin mai yin tukwane, kamar yadda Ubangiji
ya umarce ni.”*

*Yesu a gaban Bilatus*
*(Markus 15.2-5; Luka 23.3-5; Yohanna 18.33-38)*

11 Ana cikin haka, Yesu kuwa yana tsaye a gaban gwamna, sai gwamnan ya tambaye
shi, “Kai ne Sarkin Yahudawa?”
Yesu ya ce, “I, haka ne, kamar yadda ka faɗa.”
12 Da manyan firistoci da dattawa suka zarge shi, bai ba da amsa ba. 13 Sai Bilatus
ya tambaye shi ya ce, “Ba ka jin shaidar da suke kawowa a kanka?” 14 Amma Yesu
bai ce uffam game da ko ɗaya daga cikin zargin da suka yi masa ba. Har gwamna ya
yi mamaki ƙwarai.

*(Markus 15.6-15; Luka 23.13-26; Yohanna 18.39–19.16)*

* **27:10** Dubi Zak 11.12,13; Irm 19.1-13; Irm 32.6-9.

15 A wannan irin Biki, gwamna yana da wata al'ada, ta sakin ɗan kurkuku guda
wanda taron suka zaɓa. 16 To, a wannan lokaci kuwa suna da wani shahararren
ɗan kurkuku da ake kira Barabbas. 17 Saboda haka da taron suka taru, sai Bilatus
ya tambaye su ya ce, "Wane ne a cikinsu kuke so in sakar muku. Barabbas ko Yesu
wanda ake kira Kiristi?" 18 Don ya san saboda sonkai ne suka ba da Yesu a gare shi.
19 Yayinda Bilatus yake zaune a kan kujerar shari'a, sai matarsa ta aika masa da
wannan saƙo cewa, "Kada ka sa hannunka a kan marar laifin nan, domin na sha
wahala ƙwarai, a cikin mafarki yau game da shi."
20 Amma manyan firistoci da dattawa suka shawo kan taron, su ce, a ba su Barabbas,
amma a kashe Yesu.
21 Gwamna ya yi tambaya ya ce, "Wane ne cikin biyun nan, kuke so in sakar muku?"
Suka ce, "Barabbas."
22 Bilatus ya yi tambaya, "To, me zan yi da Yesu wanda ake kira Kiristi?"
Duka suka ce, "A gicciye shi!"
23 Bilatus ya ce, "Don me? Wane laifi ya yi?"
Amma suka ƙara tā da ihu, suna cewa, "A gicciye shi!"
24 Da Bilatus ya ga cewa ba ya kaiwa ko'ina, sai ma hargitsi ne yake so yǎ tashi, sai
ya ɗibi ruwa, ya wanke hannuwansa a gaban taron ya ce, "Ni kam, ba ruwana da
alhakin jinin mutumin nan. Wannan ruwanku ne!"
25 Sai dukan mutane suka amsa, suka ce, "Bari alhakin jininsa yǎ zauna a kanmu
da 'ya'yanmu!"
26 Sai ya sakar musu Barabbas. Amma ya sa aka yi wa Yesu bulala, sa'an nan ya
ba da shi a gicciye.

*Sojoji sun yi wa Yesu ba'a*
*(Markus 15.16-21; Yohanna 19.2,3)*

27 Sai sojojin gwamna suka ɗauki Yesu suka kai shi Fadar mai mulki, sa'an nan
suka tara dukan kamfanin sojoji kewaye da shi. 28 Suka tuɓe shi, suka yafa masa
wata jar riga. 29 Suka kuma tuƙa wani rawanin ƙaya, suka sa masa a kā. Suka sa
sanda a hannun damansa. Suka durƙusa a gabansa, suka yi masa ba'a, suna cewa,
"Ranka yǎ daɗe sarkin Yahudawa!" 30 Suka tattofa masa miyau, suka karɓe sandan,
suka yi ta ƙwala masa shi a kai. 31 Bayan sun yi masa ba'a, sai suka tuɓe masa rigar,
suka sa masa nasa tufafin. Sai suka tafi da shi, domin su gicciye shi.

*Gicciyewa*
*(Markus 15.16-21; Yohanna 19.2,3)*

32 Suna fitowa ke nan, sai suka sadu da wani mutumin Sairin, mai suna Siman. Sai
suka tilasta shi ya ɗauki gicciyen. 33 Sai suka iso wani wurin da ake kira Golgota
(wanda yake nufin Wurin Koƙon Kai). 34 A can, suka ba shi ruwan inabi gauraye da
wani abu mai ɗaci yǎ sha. Amma da ya ɗanɗana, sai ya ƙi sha. 35 Bayan da suka
gicciye shi, sai suka raba tufafinsa a tsakaninsu ta wurin jefa ƙuri'a. 36 Sa'an nan
suka zauna suna tsaronsa. 37 Bisa da kansa kuwa, an kafa rubutun zargin da aka yi
masa, da ya ce,

Wannan shi ne Yesu Sarkin Yahudawa.

38 An gicciye 'yan fashi biyu tare da shi, ɗaya a damansa, ɗaya kuma a hagunsa.
39 Masu wucewa, suka zazzage shi, suna kaɗa kai, 40 suna cewa, "Kai da za ka rushe
haikali, ka kuma gina shi cikin kwana uku, ceci kanka mana! In kai Ɗan Allah ne,
ka sauka daga gicciyen!"
41 Haka ma, manyan firistoci da malaman dokoki da kuma dattawa, suka yi ta yin
masa ba'a, suna cewa, 42 "Ya ceci waɗansu, amma ya kāsa ceton kansa! In shi ne
Sarkin Isra'ila! To, yǎ sauko daga kan gicciyen nan, mu kuwa mu gaskata shi. 43 Ya

dogara ga Allah. Bari Allah yă cece shi yanzu, in yana sonsa, domin ya ce, ‘Ni Ɗan
Allah ne.’ ” 44 Haka ma, ’yan fashin da aka gicciye tare da shi, suka zazzage shi.

### *Mutuwar Yesu*
### *(Markus 15.33-41; Luka 23.44-49; Yohanna 19.28-30)*

45 Daga sa’a ta shida, har zuwa sa’a ta tara, duhu ya rufe ƙasa duka. 46 Wajen sa’a
ta tara, Yesu ya ɗaga murya da ƙarfi ya ce, *“Eloi, Eloi,*† *lama sabaktani?”* (Wato, “Ya
Allahna, ya Allahna, don me ka yashe ni?”).‡
47 Sa’ad da waɗanda suke tsattsaye a wurin suka ji haka, sai suka ce, “Yana kiran
Iliya.”
48 Nan da nan, ɗaya daga cikinsu ya ruga, ya sami soso, ya jiƙa shi da ruwan tsami,
ya sa a sanda, ya miƙa wa Yesu, yă sha. 49 Sauran kuwa suka ce, “Kyale shi mu ga,
ko Iliya zai zo yă cece shi.”
50 Da Yesu ya sāke ɗaga murya da ƙarfi, sai ya saki ruhunsa.
51 A daidai wannan lokaci, sai labulen haikali ya tsage gida biyu, daga sama har
ƙasa. Kasa ta jijjiga, duwatsu kuma suka farfashe. 52 Kaburbura suka bubbuɗe,
jikunan tsarkaka da yawa kuwa cikin waɗanda da suka mutu, suka tashi. 53 Suka
firfito daga kaburbura, sa’an nan bayan tashin Yesu daga matattu, suka shiga birni
mai tsarki, suka bayyana ga mutane da yawa.
54 Da jarumin nan tare da waɗanda suke tsaron Yesu, suka ga girgizar ƙasa, da
kuma abin da ya faru, sai tsoro ya kama su, suka kuma ce, “Gaskiya, wannan Ɗan
Allah ne!”
55 Akwai mata da yawa a can, suna kallo daga nesa. Sun bi Yesu tun daga Galili,
suna masa hidima. 56 A cikinsu, akwai Maryamu Magdalin, da Maryamu uwar Yaƙub
da Yoses, da kuma uwar ’ya’yan Zebedi.

### *Bizinar Yesu*
### *(Markus 15.42-47; Luka 23.50-56; Yohanna 19.38-42)*

57 Da yamma ta yi, sai ga wani mutum mai arziki daga Arimateya, sunansa Yusuf,
wanda shi da kansa almajirin Yesu ne. 58 Ya je wurin Bilatus, ya roƙe shi yă ba shi
jikin Yesu. Sai Bilatus ya umarta a ba shi. 59 Yusuf ya ɗauki jikin ya nannaɗe shi da
zanen lilin mai tsabta. 60 Sa’an nan ya sa shi a sabon kabarinsa, wanda ya haƙa a
dutse. Bayan ya gungura wani babban dutse ya rufe bakin kabarin, sai ya tafi abinsa.
61 Maryamu Magdalin da ɗayan Maryamun, suna zaune a wurin, ɗaura da kabarin.

### *Masu gadi a kabari*

62 Kashegari, wato, bayan Ranar Shirye-shirye, sai manyan firistoci da Farisiyawa,
suka je wurin Bilatus. 63 Suka ce, “Ranka yă daɗe, mun tuna, mai ruɗin nan tun yana
da rai ya ce, ‘Bayan kwana uku, zan tashi daga matattu.’ 64 Saboda haka, ka ba da
umarni, a tsare kabarin sai rana ta uku ɗin. In ba haka ba, almajiransa za su iya
zuwa su sace jikin, sa’an nan su faɗa wa mutane cewa, an tashe shi daga matattu.
Ruɗin ƙarshen nan fa, sai yă fi na farkon muni.”
65 Sai Bilatus ya ce, “Shi ke nan, ku ɗebi soja, ku je ku tsare kabarin iya ƙoƙarinku.”
66 Sai suka je suka tsare kabarin ta wurin buga masa hatimi, suka kuma sa masu gadi.

## 28

### *Yesu ya tashi daga matattu*
### *(Markus 16.1-8; Luka 24.1-12; Yohanna 20.1-10)*

1 Bayan ranar Asabbaci, da sassafe, a ranar farko ta mako, Maryamu Magdalin tare
da ɗaya Maryamun, suka je don su ga kabarin.

† **27:46** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da Eloi, Eloi ‡ **27:46** Zab 22.1

2 Sai aka yi wata babbar girgizar ƙasa. Don wani mala'ikan Ubangiji ya sauka daga
sama, ya je kabarin, ya gungurar da dutsen, ya kuma zauna a kai. 3 Kamanninsa
yana kama da walƙiya, tufafinsa kuma fari fat kamar dusan ƙanƙara. 4 Masu gadin
kabarin kuma suka ji tsoro ƙwarai, suka yi rawan jiki, suka zama kamar matattu.
5 Mala'ikan ya ce wa matan, "Kada ku ji tsoro, domin na san cewa kuna neman
Yesu wanda aka gicciye ne. 6 Ai, ba ya nan, ya tashi kamar yadda ya faɗa. Ku zo ku
ga inda ya kwanta. 7 Sai ku tafi da sauri ku gaya wa almajiransa cewa, 'Ya tashi daga
matattu, ya kuma ya sha gabanku zuwa Galili. Can za ku gan shi.' Ga shi na faɗa
muku."
8 Sai matan suka bar kabarin da hanzari, da tsoro, sai dai cike da farin ciki, suka
tafi a guje don su gaya wa almajiransa. 9 Kwaram, sai ga Yesu ya gamu da su ya ce,
"Gaisuwa." Sai suka zo kusa da shi, suka rungumi ƙafafunsa, suka yi masa sujada.
10 Sai Yesu ya ce musu, "Kada ku ji tsoro, ku tafi ku gaya wa 'yan'uwana, su tafi Galili.
A can za su gan ni."

### *Rahoton masu gadi*

11 Yayinda matan nan suna cikin tafiya, sai waɗansu daga cikin masu gadin suka
shiga gari, suka ba wa manyan firistoci labarin duk abin da ya faru. 12 Da manyan
firistoci da dattawa suka taru, sai suka ƙulla wata dabara, suka ba wa sojojin kuɗi
mai yawa. 13 Suka ce musu, "Ku, za ku ce, 'Almajiransa ne sun zo da dare suka
sace shi, lokacin da muke barci.' 14 In wannan labari ya kai kunnen gwamna, za
mu lallashe shi, mu kuma kāre ku daga duk wata wahala." 15 Sai sojojin suka karɓi
kuɗin, suka kuma yi kamar yadda aka umarce su. Wannan labarin kuwa shi ne ake
bazawa ko'ina a cikin Yahudawa, har yǎ zuwa yau.

### *Babban umarni*
*(Markus 16.14-18; Luka 24.36-49; Yohanna 20.19-23; Ayyukan Manzanni 1.6-8)*

16 Sa'an nan almajiransa goma sha ɗaya, suka tafi Galili, suka je dutsen da Yesu
ya gaya musu. 17 Da suka gan shi, sai suka yi masa sujada, amma waɗansu suka yi
shakka. 18 Sai Yesu ya zo wurinsu ya ce, "An ba ni dukan iko a sama da kuma ƙasa.
19 Saboda haka ku tafi, ku mai da dukan al'umman duniya su zama almajiraina, kuna
yi musu baftisma a cikin*sunan Uba, da na Ɗa, da na Ruhu Mai Tsarki, 20 kuna kuma
koya musu, su yi biyayya da duk abin da na umarce ku, kuma tabbatacce, ina tare
da ku kullum, har ƙarshen zamani."

* **28:19** Ko kuwa cikin; dubi Ayy M 8.16; 19.5; Rom 6.3; 1Kor 1.13; 10.2 da Gal 3.27

# Markus

*Yohanna Mai Baftisma ya shirya hanya*
*(Mattiyu 3.1-12; Luka 3.1-18; Yohanna 1.19-28)*

1 Farkon bishara game da Yesu Kiristi, Ɗan Allah.* 2 An rubuta a cikin littafin
annabi Ishaya cewa,
“Zan aika da ɗan aikena yǎ sha gabanka,
wanda zai shirya hanyarka,”†
3 “muryar mai kira a hamada tana cewa,
‘Ku shirya wa Ubangiji hanya,
ku miƙe hanyoyi dominsa.’ ”‡
4 Ta haka Yohanna ya zo, yana baftisma a yankin hamada, yana kuma wa’azin
baftismar tuba don gafarar zunubai. 5 Dukan ƙauyukan Yahudiya da dukan mutanen
Urushalima suka fiffito zuwa wurinsa. Suna furta zunubansu, ya kuwa yi musu
baftisma a Kogin Urdun. 6 Yohanna ya sa tufafin gashin raƙumi, ya kuma yi ɗamara
da fata. Abincinsa fāri ne da kuma zumar jeji. 7 Wannan kuwa shi ne saƙonsa, “A
bayana, wanda ya fi ni iko yana zuwa, ban kuwa isa in sunkuya in kunce igiyar
takalmansa ba. 8 Ina muku baftisma da§ ruwa, amma shi zai yi muku baftisma da
Ruhu Mai Tsarki.”

*Baftisma da kuma gwajin Yesu*
*(Mattiyu 3.13-17; Luka 3.21,22)*

9 A lokacin, Yesu ya zo daga Nazaret na Galili, Yohanna kuwa ya yi masa baftisma
a Urdun. 10 Da Yesu yana fitowa daga ruwan, sai ya ga sama ya buɗe, Ruhu kuma
yana saukowa a kansa kamar kurciya. 11 Sai murya ta fito daga sama ta ce, “Kai ne
Ɗana, wanda nake ƙauna, da kai kuma nake fari ciki ƙwarai.”
12 Nan da nan, sai Ruhu ya kai shi cikin hamada, 13 ya kuma kasance a hamada
kwana arba’in, Shaiɗan yana gwada shi. Yana tare da namomin jeji, mala’iku kuma
suka yi masa hidima.

*Kiran Almajirai na farko*
*(Mattiyu 4.12-17; Luka 4.14,15)*

14 Bayan da aka sa Yohanna a kurkuku, sai Yesu ya shigo cikin Galili, yana shelar
bisharar Allah. 15 Yana cewa, “Lokaci ya yi. Mulkin Allah ya yi kusa. Ku tuba, ku
gaskata bishara!”

*(Mattiyu 4.18-22; Luka 5.1-11)*

16 Yayinda Yesu yake tafiya a gaɓar Tekun Galili, sai ya ga Siman da ɗan’uwansa
Andarawus, suna jefa abin kamun kifi a cikin tafkin, domin su masunta ne. 17 Yesu
ya ce, “Ku zo, ku bi ni, ni kuwa zan mai da ku masuntan mutane.” 18 Nan da nan,
suka bar abin kamun kifinsu, suka bi shi.
19 Da ya yi gaba kaɗan, sai ya ga Yaƙub ɗan Zebedi, da ɗan’uwansa Yohanna a
cikin jirgin ruwa, suna gyaran abin kamun kifinsu. 20 Ba da ɓata lokaci ba, ya kira
su, sai suka bar mahaifinsu Zebedi a cikin jirgin ruwan, tare da ’yan haya, suka kuwa
bi shi.

*Yesu ya fitar da mugun ruhu*
*(Luka 4.31-37)*

* **1:1** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā ba su da Ɗan Allah. † **1:2** Mal 3.1 ‡ **1:3** Ish 40.3 § **1:8** Ko kuwa a cikin

21 Suka tafi Kafarnahum. Da ranar Asabbaci ta kewayo, sai Yesu ya shiga majami'a
ya fara koyarwa. 22 Mutane suka yi mamakin koyarwarsa, domin ya koyar da su
kamar wanda yake da iko, ba kamar malaman dokoki ba. 23 Nan take, sai wani
mutum mai mugun ruhu a majami'arsu, ya ɗaga murya ya ce, 24 "Ina ruwanka da
mu, Yesu Banazare? Ka zo ne don ka hallaka mu? Na san wane ne kai, Mai Tsarki
nan na Allah!"
25 Yesu ya tsawata masa ya ce, "Yi shiru! Fita daga cikinsa!" 26 Sai mugun ruhun
ya jijjiga mutumin da ƙarfi, ya fita daga jikinsa da ihu.
27 Dukan mutane suka yi mamaki, suna tambayar juna suna cewa, "Mene ne haka?
Tabɗi! Yau ga sabuwar koyarwa kuma da iko! Yana ma ba wa mugayen ruhohi
umarni, suna kuma yin masa biyayya." 28 Labari game da shi ya bazu nan da nan
ko'ina a dukan yankin Galili.

### *Yesu ya warkar da mutane da yawa*
### *(Mattiyu 8.14-17; Luka 4.38-41)*

29 Da suka bar majami'ar, sai suka tafi gidan su Siman da Andarawus, tare da Yaƙub
da Yohanna. 30 Surukar Siman tana kwance da zazzaɓi, sai suka gaya wa Yesu game
da ita. 31 Sai ya je wajenta, ya kama hannunta, ya ɗaga ta. Zazzaɓin kuwa ya sāke
ta, ta kuma yi musu hidima.
32 A wannan yamma, bayan fāɗuwar rana, mutane suka kawo wa Yesu dukan
marasa lafiya, da masu aljanu. 33 Duk garin ya taru a ƙofar gidan. 34 Yesu kuwa ya
warkar da marasa lafiya da yawa da suke da cututtuka iri-iri. Ya kuma fitar da aljanu
da yawa, amma bai yarda aljanun suka yi magana ba, don sun san wane ne shi.

### *Yesu ya yi addu'a a wurin da ba kowa*

35 Da sassafe, tun da sauran duhu, Yesu ya tashi, ya bar gida, ya tafi wani wurin
da ba kowa, a can ya yi addu'a. 36 Siman da abokansa suka fita nemansa. 37 Da suka
same shi, sai suka ce, "Kowa yana nemanka!"
38 Yesu ya amsa ya ce, "Mu je wani wuri dabam, zuwa ƙauyukan da suke kusa, don
in yi wa'azi a can ma. Wannan shi ne dalilin zuwana." 39 Sai ya tafi ko'ina a Galili,
yana wa'azi a majami'unsu, yana kuma fitar da aljanu.

### *Mutum mai kuturta*
### *(Mattiyu 8.1-4; Luka 5.12-16)*

40 Wani mutum mai kuturta* ya zo wurinsa, ya durƙusa ya roƙe shi ya ce, "In kana
so, za ka iya tsabtacce ni."
41 Cike da tausayi, sai Yesu ya miƙa hannunsa ya taɓa mutumin ya ce, "Na yarda,
ka tsabtacce!" 42 Nan da nan, sai kuturtar ta rabu da shi, ya kuma warke.
43 Yesu ya sallame shi nan take, da gargaɗi mai ƙarfi cewa, 44 "Ka lura kada ka gaya
wa kowa wannan. Amma ka tafi ka nuna kanka ga firist, ka kuma miƙa hadayun da
Musa ya umarta saboda tsarkakewarka, don yǎ zama shaida gare su." 45 A maimakon
haka, sai ya fita, ya fara magana a sake, yana baza labarin. Saboda haka, Yesu bai
ƙara iya shiga cikin gari a fili ba, sai dai ya kasance a wuraren da ba kowa. Duk da
haka, mutane suka yi ta zuwa wurinsa daga ko'ina.

# 2

### *Yesu ya warkar da shanyayye*
### *(Mattiyu 9.1-8; Luka 5.17-26)*

1 Bayan 'yan kwanaki, da Yesu ya sāke shiga Kafarnahum, sai mutane suka ji
labarin zuwansa gida. 2 Mutane suka taru da yawa har ma babu wuri, ko a bakin ƙofa

* **1:40** Kalmar Girik da aka yi amfani da ita don kowace irin cutar da ta shafi fatar jiki ba lalle sai kuturta ba.

ma, sai ya yi musu wa'azin bishara. 3 Waɗansu mutum huɗu suka zo wajensa ɗauke
da wani shanyayye. 4 Da ba su iya kai shi wurin Yesu ba, saboda taron, sai suka buɗe
rufin gidan saman, bisa daidai inda Yesu yake. Bayan da suka huda rami, sai suka
saukar da shanyayyen, kwance a kan tabarmarsa. 5 Da Yesu ya ga bangaskiyarsu, sai
ya ce wa shanyayyen, "Saurayi, an gafarta zunubanka."
6 To, waɗansu malaman dokoki da suke zaune a wurin, suka yi tunani a zuciyarsu,
suna cewa, 7 "Me ya sa mutumin nan yake magana haka? Yana saɓo! Wane ne zai
iya gafarta zunubai, in ba Allah kaɗai ba?"
8 Nan da nan, Yesu ya gane a ruhunsa abin da suke tunani a zuciyarsu, sai ya ce
musu, "Me ya sa kuke tunanin waɗannan abubuwa? 9 Wanne ya fi sauƙi, a ce wa
shanyayyen, 'An gafarta zunubanka,' ko a ce, 'Tashi, ɗauki tabarmarka ka yi tafiya'?
10 Amma don ku san cewa, Ɗan Mutum yana da iko a duniya yǎ gafarta zunubai." Sai
ya ce wa shanyayyen, 11 "Ina ce maka, tashi, ɗauki tabarmarka, ka tafi gida." 12 Sai
ya tashi, ya ɗauki tabarmarsa, ya yi tafiyarsa a gabansu duka. Wannan ya ba wa
kowa mamaki, suka kuma ɗaukaka Allah suna cewa, "Ba mu taɓa ganin abu haka
ba!"

### *Kiran Lawi*
### *(Mattiyu 9.9-13; Luka 5.27-32)*

13 Yesu ya sāke tafiya bakin tafkin. Taro mai yawa ya zo wurinsa, sai ya fara koya
musu. 14 Yana cikin tafiya, sai ya ga Lawi, ɗan Alfayus zaune a inda ake karɓar haraji.
Yesu ya ce masa, "Bi ni." Sai Lawi ya tashi, ya bi shi.
15 Yayinda Yesu yake cin abinci a gidan Lawi, sai masu karɓar haraji da "masu
zunubi" da yawa, suka zo suka ci tare da shi da almajiransa, gama akwai mutane da
yawa da suka bi shi. 16 Da malaman dokoki, waɗanda su ma Farisiyawa ne, suka ga
yana ci tare da masu "zunubi" da masu karɓar haraji, sai suka tambayi almajiransa,
suka ce, "Me ya sa yake ci tare da masu karɓar haraji da masu zunubi?"
17 Da jin wannan, Yesu ya ce musu, "Ai, masu lafiya ba sa bukatar likita, sai dai
marasa lafiya. Ban zo domin in kira masu adalci ba, sai dai masu zunubi."

### *An tuhumi Yesu game da azumi*
### *(Mattiyu 9.14-17; Luka 5.33-39)*

18 To, almajiran Yohanna da na Farisiyawa suna azumi, sai waɗansu mutane suka
zo suka tambayi Yesu, suka ce, "Yaya almajiran Yohanna da na Farisiyawa suna
azumi, amma almajiranka ba sa yi?"
19 Yesu ya amsa ya ce, "Yaya abokan ango za su yi azumi, sa'ad da yana tare da
su? Ai, ba za su yi ba, muddin yana tare da su. 20 Ai, lokaci yana zuwa da za a ɗauke
musu angon. A sa'an nan ne fa za su yi azumi.
21 "Ba mai facin sabon ƙyalle a tsohuwar riga. In ya yi haka, sabon ƙyallen zai yage
daga tsohuwar, yagewar kuwa za tǎ zama da muni. 22 Ba wanda yakan zuba sabon
ruwan inabi a tsofaffin salkuna. In ya yi haka, ruwan inabin zai farfashe salkunan,
yǎ yi hasarar ruwan inabin, salkunan kuma su lalace. A'a, yakan zuba sabon ruwan
inabin a sababbin salkuna."

### *Ubangijin Asabbaci*
### *(Mattiyu 12.1-8; Luka 6.1-5)*

23 Wata ranar Asabbaci, Yesu yana ratsa gonakin hatsi, sai almajiransa da suke
tafiya tare da shi, suka fara kakkarya waɗansu kan hatsi. 24 Farisiyawa suka ce
masa, "Duba, me ya sa suke yin abin da doka ta hana a yi, a ranar Asabbaci?"
25 Ya amsa ya ce, "Ashe, ba ku taɓa karanta abin da Dawuda ya yi ba, sa'ad da shi
da abokan tafiyarsa suka ji yunwa, suna kuma cikin bukata? 26 Ya shiga gidan Allah a

zamanin Abiyatar babban firist, ya ci keɓaɓɓen burodin nan, ya kuma ba wa abokan
tafiyarsa abin da firistoci kaɗai sukan ci bisa ga doka?”
27 Sai ya ce musu, “An yi Asabbaci saboda mutum ne, ba mutum saboda Asabbaci
ba. 28 Don haka, Ɗan Mutum Ubangiji ne, har ma da na Asabbaci.”

# 3

*(Mattiyu 12.9-14; Luka 6.6-11)*

1 Wani lokaci, da ya sāke shiga majami’a, sai ga wani mutum mai shanyayyen
hannu. 2 Waɗansu daga cikin mutane suna neman dalilin zargin Yesu, sai suka zuba
masa ido, su ga ko zai warkar da shi a ranar Asabbaci. 3 Yesu ya ce wa mutumin mai
shanyayyen hannun, “Tashi ka tsaya a gaban kowa.”
4 Sai Yesu ya tambaye su ya ce, “Me ya kamata a yi bisa ga doka, a ranar Asabbaci,
a aikata alheri, ko a aikata mugunta, a ceci rai, ko a yi kisa?” Amma suka yi shiru.
5 Sai ya kalle su da fushi, don taurin zuciyarsu ya ɓata masa rai sosai. Sai ya ce wa
mutumin, “Miƙo hannunka.” Sai ya miƙa, hannunsa kuwa ya koma lafiyayye. 6 Sai
Farisiyawa suka fita, suka fara ƙulla shawara da mutanen Hiridus yadda za su kashe
Yesu.

### *Taron jama’a ya bi Yesu*

7 Yesu da almajiransa suka janye zuwa tafkin, taro mai yawa kuwa daga Galili ya bi
shi. 8 Mutane da yawa daga Yahudiya, da Urushalima, da Edom, da kuma yankunan
da suke ƙetaren Urdun, da kewayen Taya, da Sidon suka zo wurinsa, don sun ji
dukan abubuwan da yake yi. 9 Saboda taron, sai ya ce wa almajiransa su shirya
masa ƙaramin jirgin ruwa, don kada mutane su matse shi. 10 Gama ya warkar da
mutane da yawa, masu cututtuka suka yi ta ƙoƙarin zuwa gaba, don su taɓa shi.
11 Duk sa’ad da mugayen ruhohi suka gan shi, sai fāɗi a gabansa, su ɗaga murya, su
ce, “Kai Ɗan Allah ne.” 12 Amma yakan tsawata musu, kada su shaida ko wane ne
shi.

### *Naɗin manzanni sha biyu*
*(Mattiyu 10.1-4; Luka 6.12-16)*

13 Yesu ya hau gefen wani dutse, ya kira waɗanda yake so, suka kuma zo wurinsa.
14 Ya naɗa sha biyu, ya kira su manzanni* don su kasance tare da shi, domin kuma
yă aike su yin wa’azi, 15 don kuma su sami ikon fitar da aljanu.

16 Ga sha biyun da ya naɗa.

Siman (wanda ya ba shi suna Bitrus);
17 Yaƙub ɗan Zebedi da kuma ɗan’uwansa Yohanna (ga waɗannan kuwa ya sa musu suna Buwarnajis, wato, “’ya’yan tsawa”);
18 Andarawus,
Filibus,
Bartolomeyu,
Mattiyu,
Toma,
Yaƙub ɗan Alfayus,
Taddayus,
Siman wanda ake kira Zilot,
19 da kuma Yahuda Iskariyot, wanda ya bashe Yesu.

* **3:14** Waɗansu rubuce-rubucen hannu ba su da kira su manzanni.

### *Yesu da Be'elzebub*
*(Mattiyu 12.22-32; Luka 11.14-23; 12.10)*

20 Sai Yesu ya shiga wani gida, taro kuma ya sāke haɗuwa, har shi da almajiransa
ma ba su sami damar cin abinci ba. 21 Da 'yan'uwansa suka sami wannan labari, sai
suka tafi don su dawo da shi, suna cewa, "Ai, ya haukace."
22 Malaman dokokin da suka zo daga Urushalima suka ce, "Ai, yana da Be'elzebub†!
Da ikon sarkin aljanu yake fitar da aljanu."
23 Sai Yesu ya kira su, ya yi musu magana da misalai ya ce, "Yaya Shaiɗan zai fitar
da Shaiɗan? 24 In mulki yana gāba da kansa, wannan mulki ba zai tsaya ba. 25 In gida
yana gāba da kansa, wannan gida ba zai tsaya ba. 26 In kuwa Shaiɗan yana gāba da
kansa, ya kuma rabu biyu, ba zai tsaya ba, ƙarshensa ya zo ke nan. 27 Tabbatacce, ba
mai shiga gidan mai ƙarfi yǎ kwashe dukiyarsa, sai bayan ya daure mai ƙarfin, sa'an
nan zai iya yin fashin gidansa. 28 Gaskiya nake gaya muku, za a gafarta duk zunubai
da kuma saɓon mutane suka yi. 29 Amma duk wanda ya saɓi Ruhu Mai Tsarki, ba za
a taɓa gafara masa ba. Ya aikata madawwamin zunubi ke nan."
30 Ya faɗi haka domin suna cewa, "Yana da mugun ruhu."

### *Mahaifiyar Yesu da 'yan'uwansa*
*(Mattiyu 12.46-50; Luka 8.19-21)*

31 Sai mahaifiyar Yesu tare da 'yan'uwansa suka iso. Suna tsaye a waje, sai suka
aiki wani ciki yǎ kira shi. 32 Taron yana zaune kewaye da shi, sai suka ce masa,
"Mahaifiyarka da 'yan'uwanka suna waje, suna nemanka."
33 Ya yi tambaya ya ce, "Su wane ne mahaifiyata, da 'yan'uwana?"
34 Sai ya dubi waɗanda suke zaune kewaye da shi ya ce, "Ga mahaifiyata da
'yan'uwana! 35 Duk wanda yake aikata nufin Allah, shi ne ɗan'uwana, da 'yar'uwata,
da kuma mahaifiyata."

# 4

### *Misalin mai shuka*
*(Mattiyu 13.1-9; Luka 8.4-8)*

1 Har wa yau, Yesu ya fara koyarwa a bakin tafki. Domin taron da yake kewaye da
shi mai girma ne sosai, sai ya shiga cikin jirgin ruwa, ya zauna a ciki a tafkin, dukan
mutanen kuwa suna a gaɓar ruwan. 2 Ya koya musu abubuwa da yawa da misalai.
A koyarwarsa kuwa ya ce, 3 "Ku saurara! Wani manomi ya fita don yǎ shuka irinsa.
4 Da yana yafa irin, sai waɗansu suka fāɗi a kan hanya, tsuntsaye suka zo suka cinye
su. 5 Waɗansu suka fāɗi a wuri mai duwatsu inda babu ƙasa sosai. Nan da nan, suka
tsira domin ƙasar ba zurfi. 6 Amma da rana ta taso, sai tsire-tsiren suka ƙone, suka
yanƙwane, domin ba su da saiwa. 7 Waɗansu irin suka fāɗi a cikin ƙaya. Da suka
yi girma sai ƙaya suka shaƙe su, har ya sa ba su yi ƙwaya ba. 8 Har yanzu, waɗansu
irin suka fāɗi a ƙasa mai kyau. Suka tsira, suka yi girma, suka ba da amfani, suka yi
riɓi talatin-talatin, waɗansu sittin-sittin, waɗansu kuma ɗari-ɗari."
9 Sai Yesu ya ce, "Duk mai kunnen ji, yǎ ji."
*(Mattiyu 13.10-17; Luka 8.9,10)*
10 Lokacin da yake shi kaɗai, Sha Biyun, da kuma waɗanda suke kewaye da shi,
suka tambaye shi game da misalan. 11 Sai ya ce musu, "An ba ku sanin asirin mulkin
Allah. Amma ga waɗanda suke waje kuwa, kome sai da misalai. 12 Saboda,
" 'ko sun dinga duba, ba za su taɓa gane ba,
kuma ko su dinga ji, ba za su taɓa fahimta ba,

† **3:22** Girik Be'ezebowul ko Be'elzebowul

in ba haka ba, mai yiwuwa, su tuba, a gafarta musu!’ ”*
*(Mattiyu 13.18-23; Luka 8.11-15)*
13 Sai Yesu ya ce musu, “Ba ku fahimci wannan misali ba? Yaya za ku fahimci
wani misali ke nan? 14 Manomi yakan shuka maganar Allah. 15 Waɗansu mutane
suna kama da irin da ya fāɗi a kan hanya, inda akan shuka maganar Allah. Da
jin maganar, nan da nan sai Shaiɗan yă zo yă ɗauke maganar da aka shuka a
zuciyarsu. 16 Waɗansu suna kama da irin da aka shuka a wurare masu duwatsu,
sukan ji maganar Allah, sukan kuma karɓe ta nan da nan da farin ciki. 17 Amma da
yake ba su da saiwa, ba sa daɗewa. Da wahala ko tsanani ya tashi saboda maganar,
nan da nan, sai su ja da baya. 18 Har yanzu, waɗansu kamar irin da aka shuka
cikin ƙaya, sukan ji maganar, 19 amma damuwar wannan duniya, da son dukiya, da
kuma kwaɗayin waɗansu abubuwa, sukan shiga, su shaƙe maganar, har su mai da
ita marar amfani. 20 Waɗansu mutane kuwa suna kama da irin da aka shuka a ƙasa
mai kyau, sukan ji maganar Allah, su kuma karɓa, sa’an nan kuma su fid da amfani
riɓi talatin-talatin, ko sittin-sittin, ko ɗari-ɗari.”

*Fitila a kan wurin ajiye fitila*
*(Luka 8.16-18)*
21 Sai ya ce musu, “Ko kukan kawo fitila ku rufe ta da murfi ko kuma ku sa ta a
ƙarƙashin gado ne? Ba kukan sa ta a kan wurin ajiye fitila ba? 22 Duk abin da yake
a ɓoye, dole za a fallasa shi. Duk abin da kuma yake a rufe, dole za a fitar da shi a
fili. 23 Duk mai kunnen ji, bari yă ji.”
24 Ya ci gaba da cewa, “Ku lura da abin da kuke ji da kyau. Mudun da ka auna da
shi, da shi za a auna maka, har ma a ƙara. 25 Duk wanda yake da shi, za a ƙara masa,
duk wanda kuma ba shi da shi, ko abin da yake da shi ma, za a karɓe daga gare shi.”

*Misalin irin da ya tsiro*
26 Ya sāke cewa, “Mulkin Allah yana kama da haka. Wani mutum ya yafa iri a
gona. 27 A kwana a tashi har irin yă tsiro, yă yi girma, bai kuwa santa yadda aka yi
ba. 28 Kasar da kanta takan ba da ƙwaya, da farko takan fid da ƙara, sa’an nan ta
fid da kai, sa’an nan kan yă fid da ƙwaya. 29 Da ƙwayan ya nuna, sai yă sa lauje yă
yanka, domin lokacin girbi ya yi.”

*Misalin ƙwayar mustad*
*(Mattiyu 13.31,32; Luka 13.18,19)*
30 Ya kuma ce, “Da me za mu kwatanta mulkin Allah, ko kuwa da wane misali za mu
bayyana shi? 31 Yana kama da ƙwayar mustad, wadda ita ce ƙwaya mafi ƙanƙanta
da akan shuka a gona. 32 Duk da haka, in aka shuka ƙwayar, sai tă yi girma, tă
zama mafi girma a itatuwan lambu. Har itacen yă kasance da manyan rassa, inda
tsuntsayen sararin sama sukan iya huta a inuwarsa.”
*(Mattiyu 13.34,35)*
33 Da misalai da yawa irin waɗannan, Yesu ya yi magana da su, daidai yadda za su
iya fahimta. 34 Ba abin da ya faɗa musu, da ba da misali ba. Amma lokacin da yake
shi kaɗai tare da almajiransa, sai yă bayyana kome.

*Yesu ya kwantar da iska*
*(Mattiyu 8.23-27; Luka 8.22-25)*
35 A wannan rana, da yamma, sai ya ce wa almajiransa, “Mu ƙetare zuwa wancan
hayi.” 36 Da suka bar taron, sai suka tafi tare da shi yadda yake, a cikin jirgin ruwa.
Akwai waɗansu jiragen ruwa kuma tare da shi. 37 Sai babban hadari mai iska ya
tashi, raƙuman ruwa suna ta bugun jirgin ruwan, har jirgin ruwan ya kusa yă cika

* **4:12** Ish 6.9,10

da ruwa. 38 Yesu kuwa yana can baya, yana barci a kan katifa. Sai almajiran suka
tashe shi suka ce masa, “Malam, ba ka kula ba ko mu nutse?”
39 Sai ya farka ya tsawata wa iskar, ya ce wa raƙuman ruwan, “Shiru! Ku natsu!”
Sai iskar ta kwanta, kome kuma ya yi tsit.
40 Sai ya ce wa almajiransa, “Don me kuke tsoro haka? Har yanzu ba ku da
bangaskiya ne?”
41 Suka tsorata, suka ce wa juna, “Wane ne wannan? Har iska da raƙuman ruwa
ma suna masa biyayya!”

# 5

*Warkar da mai aljanu*
*(Mattiyu 8.28-34; Luka 8.26-39)*

1 Suka ƙetare tafkin suka je yankin Gerasenawa.* 2 Da Yesu ya sauka daga jirgin
ruwa, sai wani mutum mai mugun ruhu ya fito daga kaburbura, ya tarye shi.
3 Wannan mutumin ya mai da kaburbura gidansa. Kuma ba wanda ya iya daure
shi, ko da sarƙa ma. 4 Gama an sha daure shi hannu da ƙafa da sarƙa, amma yakan
tsintsinke sarƙar, yă kuma karye ƙarafan da suke ƙafafunsa. Ba wanda yake da
ƙarfin da zai iya yă riƙe shi. 5 Dare da rana, sai yă dinga kuka yana ƙuƙƙuje jikinsa
da duwatsu a cikin kaburbura da kan tuddai.
6 Da ya hangi Yesu daga nesa, sai ya ruga da gudu, ya zo ya durƙusa a gabansa. 7 Ya
yi ihu da babbar murya ya ce, “Ina ruwanka da ni Yesu, Ɗan Allah Mafi Ɗaukaka?
Ka rantse da Allah cewa ba za ka ba ni azaba ba!” 8 Gama Yesu ya riga ya ce masa,
“Ka fita daga jikin mutumin nan, kai mugun ruhu!”
9 Sai Yesu ya tambaye shi ya ce, “Mene ne sunanka?”
Sai ya amsa ya ce, “Sunana Lejiyon, wato, ‘Tuli,’ domin muna da yawa.” 10 Sai ya
yi ta roƙon Yesu, kada yă kore su daga wurin.
11 A kan tudun da yake nan kusa kuwa, akwai wani babban garken aladu, suna
kiwo. 12 Sai aljanun suka roƙi Yesu, suka ce, “Tura mu cikin aladun nan, ka bari mu
shiga cikinsu.” 13 Ya kuwa yarda musu, sai mugayen ruhohin suka fita suka shiga
cikin aladun. Garken kuwa, yana da kusan aladu dubu biyu, suka gangara daga kan
tudun zuwa cikin tafkin, suka nutse.
14 Masu kiwon aladun kuwa suka ruga da gudu zuwa cikin gari da ƙauyuka, suka
ba da wannan labari. Sai mutanen suka fito, domin su ga abin da ya faru. 15 Da suka
kai wajen Yesu, sai suka ga mutumin da dā yake da tulin aljanun yana zaune a wurin,
sanye da tufafi kuma cikin hankalinsa, sai suka ji tsoro. 16 Waɗanda suka ga abin da
ya faru, suka ba da labarin abin da ya faru da mai aljanun, da kuma aladun. 17 Sai
mutane suka fara roƙon Yesu yă bar yankinsu.
18 Yesu yana kan shiga cikin jirgin ruwa ke nan, sai mutumin da dā yake da aljanun
ya roƙa yă bi shi. 19 Yesu bai yardar masa ba, amma ya ce, “Ka tafi gida wurin iyalinka,
ka gaya musu babban alherin da Ubangiji ya yi maka, da yadda ya yi maka jinƙai.”
20 Sai mutumin ya tafi, ya yi ta ba da labari a cikin Dekafolis† a kan babban alherin
da Yesu ya yi masa. Dukan mutane kuwa suka yi mamaki.

*Yarinya da ta mutu da mace marar lafiya*
*(Mattiyu 9.18-26; Luka 8.40-56)*

21 Da Yesu ya sāke ƙetarewa cikin jirgin ruwa zuwa ɗaya hayen tafkin, sai taro mai
yawa ya taru kewaye da shi yayinda yake a bakin tafkin. 22 Sai ɗaya a cikin masu
mulkin majami'a, wanda ake kira Yayirus ya zo wurin. Da ganin Yesu, sai ya durƙusa

* **5:1** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da Gadarenes; Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da Gergesenes † **5:20** Wato, Birane Goma

a gabansa, 23 ya roƙe shi da gaske ya ce, “Karamar diyata tana bakin mutuwa. In ka
yarda, ka zo ka ɗibiya hannunka a kanta, domin ta warke, ta kuma rayu.” 24 Sai Yesu
ya tafi tare da shi.

Babban taron kuma ya bi shi, suna ta matsinsa a kowane gefe. 25 A can kuwa
akwai wata mace, wadda ta yi shekaru goma sha biyu tana zub da jini. 26 Ta kuma
sha wahala ƙwarai a hannun likitoci da yawa, har ta kashe duk abin da take da shi,
amma maimakon samun sauƙi, sai ciwon ya ƙara muni. 27 Da ta ji labarin Yesu, sai
ta zo ta bayansa, a cikin taron, ta taɓa rigarsa, 28 domin ta yi tunani cewa, “Ko da
rigunarsa ma na taɓa, zan warke.” 29 Nan da take, zub da jininta ya tsaya, sai ta ji a
jikinta ta rabu da shan wahalarta.

30 Nan da nan Yesu ya gane cewa, iko ya fita daga gare shi. Sai ya juya a cikin taron
ya yi tambaya, “Wa ya taɓa rigata?”

31 Sai almajiransa suka ce, “Kana ganin mutane suna matsinka, duk da haka kana
tambaya, ‘Wa ya taɓa ni?’ ”

32 Amma Yesu ya ci gaba da dubawa don yă ga wa ya taɓa shi. 33 Matar, da yake ta
san abin da ya faru da ita, sai ta zo ta durƙusa a gabansa, da tsoro da rawan jiki, ta
kuma gaya masa dukan abin da ya faru. 34 Sai ya ce mata, “Diyata, bangaskiyarki ta
warkar da ke. Ki sauka lafiya, kin kuma rabu da dukan wahalarki.”

35 Yayinda Yesu yana cikin magana, sai waɗansu mutane daga gidan Yayirus, mai
mulkin majami’a, suka zo suka ce, “Diyarka ta rasu. Kada ma ka wahal da Malam.”

36 Yesu bai kula da abin da suka faɗa ba, sai ya ce wa mai mulkin majami’ar, “Kada
ka ji tsoro, ka gaskata kawai.”

37 Bai bar kowa ya bi shi ba, sai Bitrus, Yaƙub da Yohanna ɗan’uwan Yaƙub. 38 Da
suka iso gidan mai mulkin majami’ar, sai Yesu ya ga ana hayaniya, mutane suna kuka
da kururuwa. 39 Sai ya shiga ciki, ya ce musu, “Mene ne dalilin wannan hayaniya da
kuka? Yarinyar ba mutuwa ne ta yi ba, barci take yi.” 40 Sai suka yi masa dariya.

Bayan ya fitar da su duk waje, sai ya ɗauki mahaifin da mahaifiyar yarinyar tare da
almajiran da suke tare da shi, suka shiga inda yarinyar take. 41 Sai ya kama hannunta
ya ce mata, *“Talita kum!”* (Wato, “Karamar yarinya, na ce miki, tashi!”). 42 Nan da
nan, sai yarinyar ta tashi ta yi tafiya (shekarunta goma sha biyu ne). Saboda wannan,
suka yi mamaki ƙwarai. 43 Sai ya ba da umarni mai tsanani, kada kowa yă san kome
game da wannan. Sai ya ce musu, su ba ta wani abu tă ci.

# 6

### *Annabi marar daraja*
### *(Mattiyu 13.53-58; Luka 4.16-30)*

1 Yesu ya tashi daga can ya tafi garinsa, tare da almajiransa. 2 Da Asabbaci ya
kewayo, sai ya fara koyarwa a cikin majami’a, mutane da yawa da suka saurare shi,
suka yi mamaki.

Suna tambaya, “Ina mutumin nan ya sami waɗannan abubuwa? Wace hikima ce
wannan da aka ba shi, har da yana yin ayyukan banmamaki haka! 3 Ashe, wannan
ba shi ne kafinta nan ba? Shin, ba shi ne ɗan Maryamu ba, ba shi ne ɗan’uwan su
Yaƙub, Yusuf, Yahuda da kuma Siman ba? Ashe, ’yan’uwansa mata kuma ba suna
nan tare da mu ba?” Sai suka ji haushinsa.

4 Yesu ya ce musu, “Sai a garinsa kaɗai, da kuma cikin ’yan’uwansa, da cikin
gidansa ne, annabi ba shi da daraja.” 5 Bai iya yin ayyukan banmamaki a wurin
ba, sai dai ɗibiya hannuwansa da ya yi a kan mutane kima da suke da cututtuka, ya
kuwa warkar da su. 6 Ya kuwa yi mamaki ƙwarai don rashin bangaskiyarsu.

### *Yesu ya aiki sha biyun*
### *(Mattiyu 10.5-15; Luka 9.1-6)*

Sai ya Yesu zazzaga ƙauyuka yana koyarwa. 7 Ya kira Sha Biyun nan wurinsa, ya
aike su biyu-biyu, ya kuma ba su iko bisa mugayen ruhohi.
8 Ga dai umarnansa, “Kada ku ɗauki kome don tafiyar, sai dai sanda ba burodi,
ba jaka, ba kuɗi a ɗamararku. 9 Ku sa takalma, amma ban da riga fiye da waɗanda
kuka sa. 10 Duk sa’ad da kuka shiga wani gida, ku zauna nan sai kun bar garin. 11 In
kuwa a wani wuri ba a karɓe ku, ba a kuwa saurare ku ba, sai ku karkaɗe ƙurar
ƙafafunku sa’ad da kuka fita, a matsayin shaida a kansu.”
12 Suka fita, suna yi wa’azi, suna ce wa mutane su tuba. 13 Suka fitar da aljanu da
yawa, suka shafa wa marasa lafiya da yawa mai, suka kuwa warkar da su.

### *An yanke kan Yohanna Mai Baftisma*
### *(Mattiyu 14.1-12; Luka 9.7-9)*

14 Sarki Hiridus ya ji wannan labari, gama sunan Yesu ya bazu a ko’ina. Waɗansu
suna cewa, “An tashe Yohanna Mai Baftisma daga matattu ne, shi ya sa yana da ikon
yin ayyukan banmamakin nan.”
15 Waɗansu suka ce, “Ai, Iliya ne.”
Har wa yau waɗansu suka ce, “Ai, annabi ne, kamar ɗaya daga cikin annabawan
dā.”
16 Amma da Hiridus ya ji haka, sai ya ce, “Ai, Yohanna ne, mutumin da na yanke
masa kai, shi ne ya tashi daga matattu!”
17 Gama Hiridus da kansa ya ba da umarni a kama Yohanna, ya kuma sa aka daure
shi, aka sa shi a kurkuku. Ya yi haka saboda Hiridiyas, matar ɗan’uwansa Filibus,
wadda ya aura. 18 Gama Yohanna ya yi ta ce wa Hiridus, “Ba daidai ba ne bisa ga
doka, ka ɗauki matar ɗan’uwanka.” 19 Saboda haka, Hiridiyas ta ƙulla munafunci
game da Yohanna, ta kuma so ta kashe shi. Amma ba tă iya ba, 20 domin Hiridus yana
jin tsoron Yohanna, ya kuma kāre shi sosai, da sanin cewa shi mutum ne mai adalci
da kuma mai tsarki. Duk sa’ad da Hiridus ya saurari Yohanna, yakan damu ƙwarai,
duk da haka, yakan so yă ji shi.
21 A ƙarshe, ta sami zarafi. A ranar murnar haihuwar Hiridus, ya yi biki domin
hakimansa, da shugabannin sojojinsa, da kuma manyan mutanen Galili. 22 Sa’ad da
diyar Hiridiyas ta shigo, ta kuma yi rawa, sai ta gamshi Hiridus tare da baƙinsa.
Sai Sarkin ya ce wa yarinyar, “Ki tambaye ni kome da kike so, ni kuwa zan ba ki.”
23 Ya yi mata alkawari da rantsuwa cewa, “Duk abin da kika roƙa, zan ba ki, ko da
rabin mulkina ne.”
24 Sai ta fita ta ce wa mahaifiyarta, “Me zan roƙa?”
Ta ce, “Kan Yohanna Mai Baftisma.”
25 Nan da nan, sai yarinyar ta yi hanzari zuwa wajen sarki da roƙon, “Ina so ka ba
ni kan Yohanna Mai Baftisma a cikin tasa, yanzu-yanzu nan.”
26 Sai sarki ya yi baƙin ciki ƙwarai, amma saboda rantsuwar da kuma baƙinsa, bai
so yă hana ta ba. 27 Nan take, sai ya aiki mai aiwatar da kisa da umarni ya kawo kan
Yohanna. Mutumin ya je ya yanke kan Yohanna a kurkuku. 28 Ya kuma kawo kan a
tasa ya ba yarinyar. Ita kuma ta ba wa mahaifiyarta. 29 Da almajiran Yohanna suka
sami labari, sai suka zo suka ɗauki jikinsa suka binne a kabari.

### *Yesu ya ciyar da dubu biyar*
### *(Mattiyu 14.13-21; Luka 9.10-17; Yohanna 6.1-14)*

30 Manzannin suka taru kewaye da Yesu, suka ba shi rahoton duk abin da suka yi,
da kuma suka koyar. 31 To, saboda mutane da yawa suna kai da kawowa, har ma ba

su sami damar cin abinci ba, sai ya ce musu, “Ku zo mu kaɗaita inda ba kowa don ku ɗan huta.”
[32] Sai suka tafi a jirgin ruwa su kaɗai, inda ba kowa. [33] Amma mutane da yawa
waɗanda suka ga tashinsu, sun gane su, sai suka ruga da gudu a ƙafa daga dukan
birane, suka riga su kaiwa can. [34] Da Yesu ya sauka, ya ga taro mai yawa, sai ya ji
tausayinsu, gama kamar tumaki suke waɗanda ba su da makiyayi. Sai ya fara koya
musu abubuwa da yawa.
[35] A lokacin nan yamma ta yi, sai almajiransa suka zo wurinsa suka ce masa, “Wurin
nan ƙauye ne, ga shi kuma lokaci ya ƙure. [36] Ka sallami mutanen su shiga ƙauyukan
da suke kurkusa, su sayi wa kansu wani abu, su ci.”
[37] Sai ya amsa ya ce, “Ku, ku ba su wani abu su ci.”

Suka ce masa, “Ai, wannan zai ɗauki albashin wata takwas na mutum!* Mu je mu
kashe yawan kuɗin nan a burodi mu ba su su ci?”
[38] Sai ya yi tambaya ya ce, “Burodi nawa kuke da su? Je ku duba.”

Da suka duba, sai suka ce, “Biyar da kifi biyu.”
[39] Sa’an nan Yesu ya umarce su su sa dukan mutanen su zazzauna ƙungiya-ƙungiya
a kan ɗanyar ciyawa. [40] Haka suka zazzauna a ƙungiyar ɗari-ɗari, da kuma hamsin-
hamsin. [41] Ya ɗauki burodi guda biyar da kifin nan biyu, ya ɗaga kai sama, ya yi
godiya, ya kakkarya burodin. Sai ya ba wa almajiransa su rarraba wa mutane. Ya
kuma rarraba kifi biyun a tsakaninsu duka. [42] Kowa ya ci, ya ƙoshi, [43] almajiran suka
kwashe gutsattsarin burodin da na kifin cike da kwanduna goma sha biyu. [44] Yawan
mutanen da suka ci kuwa maza dubu biyar ne.

### *Yesu ya yi tafiya kan ruwa*
### *(Mattiyu 14.22-33; Yohanna 6.15-21)*

[45] Nan da nan Yesu ya sa almajiransa su shiga jirgin ruwa, su sha gabansa zuwa
Betsaida, shi kuma yă sallami taron. [46] Bayan ya bar su, sai ya hau kan dutse don yă
yi addu’a.
[47] Da yamma ta yi, jirgin ruwan yana tsakiyar tafkin, Yesu kuma yana can a ƙasa
shi kaɗai. [48] Ya ga almajiran suna ƙama da tuƙi saboda iska tana gāba da su. Wajen
tsara ta huɗu na dare, sai ya tafi wurinsu, yana takawa a kan tafkin. Ya yi kamar zai
wuce su, [49] amma da suka gan shi yana takawa a kan tafkin, sai suka yi tsammani
fatalwa ce. Sai suka yi ihu, [50] domin dukansu sun gan shi, suka kuma tsorata.

Nan da nan ya yi magana da su ya ce, “Ku yi ƙarfin hali! Ni ne. Kada ku ji tsoro.”
[51] Sai ya shiga jirgin ruwan tare da su, iskar kuma ta kwanta. Dukansu suka yi
mamaki, [52] gama ba su fahimci al’amarin burodin nan ba, don zuciyarsu ta taurare.

### *(Mattiyu 14.34-36)*

[53] Da suka haye, sai suka sauka a Gennesaret, suka daure jirgin a ƙugiya. [54] Da
fitowarsu daga jirgin, sai mutane suka gane Yesu. [55] Suka gama yankin da gudu,
suna ɗaukan marasa lafiya a kan tabarmai zuwa duk inda suka ji yake. [56] Duk inda
ya shiga, cikin ƙauyuka, birane ko karkara, sai su kwantar da marasa lafiya a bakin
kasuwa. Suka roƙe shi yă bari su taɓa gefen rigarsa kawai, kuma duk waɗanda suka
taɓa shi kuwa, suka warke.

## 7

### *Mai tsabta da marar tsabta*
### *(Mattiyu 15.1-9)*

[1] Farisiyawa da waɗansu malaman dokoki waɗanda suka zo daga Urushalima, suka
taru kewaye da Yesu. [2] Sai suka ga waɗansu daga cikin almajiransa suna cin abinci da

* **6:37** Girik zai ci dinari ɗari biyu

hannuwa marasa tsabta, wato, da ba a wanke ba. 3 (Farisiyawa da dukan Yahudawa
ba sa cin abinci, sai sun wanke hannuwa sarai tukuna, yadda al’adun dattawa suka
ce. 4 Sa’ad da suka dawo daga wurin kasuwanci, dole su wanke hannu kafin su ci
abinci. Sukan kuma kiyaye waɗansu al’adu da yawa, kamar wanken kwafuna, tuluna
da butoci.*)
5 Saboda haka, Farisiyawa da malaman dokoki suka tambayi Yesu, suka ce, “Don
me almajiranka ba sa bin al’adun dattawa, a maimakon haka suna cin abinci da
hannuwa marasa tsabta?”
6 Ya amsa ya ce, “Daidai ne Ishaya ya yi annabci game da ku munafukai; kamar
yadda yake a rubuce cewa,
“ ‘Waɗannan mutane da baki suke girmama ni,
amma zukatansu sun yi nesa da ni.
7 A banza suke mini sujada,
koyarwarsu, dokokin mutane ne kawai.’†
8 Kun yar da umarnan Allah, kuna bin al’adun mutane.”
9 Ya kuma ce musu, “Kuna da hanya mai sauƙi na ajiye umarnan Allah a gefe
ɗaya, don ku kiyaye al’adunku! 10 Gama Musa ya ce, ‘Ka girmama mahaifinka da
mahaifiyarka,’‡kuma, ‘Duk wanda ya zagi mahaifinsa ko mahaifiyarsa, dole a kashe
shi.’§ 11 Amma ku, kukan ce, in mutum ya ce wa mahaifinsa, ko mahaifiyarsa, ‘Duk
taimakon da ya kamata ku samu daga wurina, Korban ne,’ (wato, abin da aka keɓe wa
Allah), 12 sa’an nan haka ba kwa ƙara barinsa yă yi wa mahaifinsa ko mahaifiyarsa
wani abu. 13 Ta haka kuke rushe maganar Allah ta wurin al’adun da kuke miƙa wa
’ya’yanku. Haka kuma kuke yin abubuwa da yawa.”

*(Mattiyu 15.10-20)*

14 Sai Yesu ya sāke kiran taron wurinsa ya ce, “Ku saurare ni dukanku, ku kuma
fahimci wannan. 15 Ba abin da yake shiga mutum daga waje ba ne yake ƙazantar da
shi. Sai dai abin da ya fita daga cikin mutum ne, yake ƙazantar da shi.”*
17 Bayan ya bar taron, ya shiga gida, sai almajiransa suka tambaye shi ma’anar
wannan misali. 18 Ya ce, “Ashe, ba ku da saurin ganewa? Ba ku gane cewa ba abin
da yake shiga mutum daga waje ba ne yake ƙazantar da shi. 19 Gama ba ya shiga
cikin zuciyarsa, sai dai cikin tumbinsa, sa’an nan kuma yă fita daga jikinsa.” (Da
faɗin haka, Yesu ya nuna tsabtar kowane irin abinci.)
20 Ya ci gaba, “Abin da yake fitowa daga mutum ne yake ƙazantar da shi. 21 Gama
daga ciki, daga zuciyar mutane, mugayen tunani suke fitowa, fasikanci, sata, kisankai,
zina, 22 kwaɗayi, ƙeta, ruɗu, ƙazantaccen sha’awa, kishi, ɓata suna, girman kai da
kuma wauta. 23 Duk waɗannan mugayen abubuwa daga cikin suke fitowa, suna
kuma ƙazantar da mutum.”

### *Bangaskiyar Baheleniya*
*(Mattiyu 15.21-28)*

24 Sai Yesu ya bar wurin, ya kuma tafi wajajen Taya. Ya shiga wani gida, bai kuwa so
kowa yă sani ba. Duk da haka, bai iya ɓoye kasancewarsa ba. 25 Da jin labarinsa, sai
wata mace wadda ƙaramar diyarta tana da mugun ruhu, ta zo ta durƙusa a gabansa.
26 Macen kuwa mutuniyar Hellenawa ce, an haife ta a Funisiya a Suriya. Ta roƙi Yesu
yă fitar da aljani da yake jikin diyarta.
27 Yesu ya ce mata, “Da farko, bari ’ya’ya su ci su ƙoshi tukuna, gama ba daidai ba
ne, a ɗauki burodin yara a jefa wa karnukansu.”

* **7:4** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na farko-farko suna da tuluna, butoci da kujeru † **7:7** Ish 29.13 ‡ **7:10** Fit 20.12; M Sh 5.16 § **7:10** Fit 21.17; Fir 20.9 * **7:15** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na farko-farko suna da “marar tsabta.” 16 Duk mai kunnuwan ji, yă ji

28 Ta amsa, ta ce, “I, Ubangiji, ko karnuka ma da suke ƙarƙashin tebur, sukan ci
burbuɗin da suke fāɗuwa daga abincin yara.”
29 Sai ya ce mata, “Saboda irin wannan amsa, ki tafi, aljanin ya rabu da diyarki.”
30 Ta tafi gida, ta tarar da diyarta kwance a gado, aljanin kuwa ya fita.

### *Warkar da kurma wanda yake kuma bebe*

31 Sai Yesu ya bar wajajen Taya, ya bi ta Sidon har zuwa Tekun Galili da kuma cikin
yankin Dekafolis.† 32 A can ne waɗansu mutane suka kawo masa wani kurma, wanda
da ƙyar yake magana. Sai suka roƙe shi yǎ ɗibiya hannunsa a kan mutumin.
33 Bayan da ya jawo shi gefe, sai Yesu ya sa yatsotsinsa a kunnuwan mutumin, ya
tofa miyau ya kuma taɓa harshen mutumin. 34 Ya ɗaga kai sama, ya ja numfashi mai
zurfi, sa’an nan ya ce masa, *“Effata!”* (Wato, “Buɗe!”). 35 Bayan ya faɗa haka, sai
kunnuwan mutumin suka buɗe, harshensa kuma ya kunce, sai ya fara magana sarai.
36 Yesu ya umarce su, kada su gaya wa kowa. Amma ƙara yawan kwaɓarsu ƙara
yawan yaɗa labarin suke ta yi. 37 Mutane suka cika da mamaki, suka ce, “Kai, ya yi
kome daidai. Har ma yana sa kurame su ji, bebaye kuma su yi magana.”

# 8

### *Yesu ya ciyar da dubu huɗu*
*(Mattiyu 15.32-39)*

1 A kwanakin nan wani taro mai girma ya taru. Tun da yake ba su da abin da za
su ci, sai Yesu ya kira almajiransa ya ce, 2 “Ina jin tausayin mutanen nan, kwanansu
uku ke nan tare da ni, kuma ba su da abin da za su ci. 3 In na sallame su gida da
yunwa, za su kāsa a hanya, don waɗansu daga cikinsu sun zo daga nesa.”
4 Almajiransa suka amsa suka ce, “Amma a ina, a wannan wurin da ba kowa, wani
zai iya samun isashen burodi, don a ciyar da su?”
5 Sai Yesu ya yi tambaya ya ce, “Burodi guda nawa kuke da su?”
Suka ce, “Bakwai.”
6 Sai ya gaya wa taron su zazzauna a ƙasa. Bayan ya ɗauki burodin nan bakwai,
ya yi godiya, sai ya kakkarya, ya ba wa almajiransa su rarraba wa mutanen, suka
kuwa yi haka. 7 Suna kuma da ƙananan kifaye kaɗan, ya ba da godiya dominsu, ya
kuma ce wa almajiran su rarraba musu. 8 Mutanen suka ci, suka ƙoshi. Daga baya,
almajiran suka tattara gutsattsarin da suka rage cike da kwanduna bakwai. 9 Wajen
maza dubu huɗu ne suka kasance. Da ya sallame su, 10 sai ya shiga jirgin ruwa tare
da almajiransa, suka tafi yankin Dalmanuta.

*(Mattiyu 16.1-4)*

11 Farisiyawa suka zo suka fara yin wa Yesu tambayoyi. Don su gwada shi, sai suka
nemi yǎ nuna musu wata alama daga sama. 12 Sai ya ja numfashi mai zurfi ya ce,
“Don me wannan zamani yake neman ganin abin banmamaki? Gaskiya nake gaya
muku, ba wata alamar da za a ba su.” 13 Sai ya bar su, ya koma cikin jirgin ruwan,
suka ƙetare zuwa ɗaya hayin.

### *Yistin Farisiyawa da na Hiridus*
*(Mattiyu 16.5-12)*

14 Almajiran suka manta su riƙe burodi, sai dai guda ɗaya da suke da shi a cikin
jirgin ruwan. 15 Yesu ya gargaɗe su ya ce, “Ku yi hankali, ku kuma lura da yistin
Farisiyawa da na Hiridus.”
16 Suka tattauna wannan da juna, suna cewa, “Don ba mu da burodi ne.”

---

† **7:31** Wato, Birane Goma

17 Da ya gane abin da suke tattaunawa, sai Yesu ya tambaye su ya ce, “Don me
kuke zancen rashin burodi? Har yanzu ba ku gane ko fahimta ba? Zukatanku sun
taurare ne? 18 Kuna da idanu, amma kun kāsa gani, kuna da kunnuwa, amma kun
kāsa ji? Ba ku tuna ba? 19 Da na kakkarya burodi guda biyar wa mutane dubu biyar,
kwanduna nawa kuka kwashe cike da gutsattsarin?”
Suka amsa, “Sha biyu.”
20 “Da na kuma kakkarya burodin nan bakwai wa mutum dubu huɗu, kwanduna
nawa kuka kwashe cike da gutsattsarin?”
Suka ce, “Bakwai.”
21 Ya ce musu, “Har yanzu ba ku fahimta ba?”

### *An warkar da makaho*

22 Suka iso Betsaida, sai waɗansu mutane suka kawo wani makaho, suka roƙi Yesu
yă taɓa shi. 23 Yesu ya kama hannun makahon ya kai shi bayan ƙauyen. Bayan ya
tofa miyau a idanun mutumin, ya kuma ɗibiya masa hannuwansa, sai ya tambaye
shi ya ce, “Kana iya ganin wani abu?”
24 Sai ya ɗaga kai ya ce, “Ina ganin mutane, suna kama da itatuwa da suke tafiya.”
25 Yesu ya sāke ɗibiya hannuwansa a idanun mutumin, sai idanunsa suka buɗe, ya
sami gani, ya kuma ga kome sarai. 26 Yesu ya sallame shi gida ya ce, “Kada ka shiga
cikin ƙauyen.”*

### *Shaidar Bitrus a kan Kiristi*
*(Mattiyu 16.13-20; Luka 9.18-21)*

27 Yesu da almajiransa suka tafi ƙauyukan da suke kewaye da Kaisariya Filibbi. A
hanya ya tambaye su ya ce, “Wa, mutane suke ce da ni?”
28 Suka amsa, suka ce, “Waɗansu suna cewa, Yohanna Mai Baftisma, waɗansu Iliya,
waɗansu kuma har wa yau sun ce, ɗaya daga cikin annabawa.”
29 Sai ya yi tambaya ya ce, “Amma ku fa, wa kuke ce da ni?”
Bitrus ya amsa ya ce, “Kai ne Kiristi.†”
30 Yesu ya gargaɗe su kada su gaya wa kowa kome a kansa.

### *Yesu ya yi zancen mutuwarsa*
*(Mattiyu 16.21-28; Luka 9.22-27)*

31 Sai ya fara koya musu cewa, dole Ɗan Mutum yă sha wahaloli da yawa, dattawa,
manyan firistoci da malaman dokoki kuma su ƙi shi. Dole kuma a kashe shi, bayan
kwana uku kuma, yă tashi. 32 Ya yi wannan zance a sarari. Sai Bitrus ya jawo shi
gefe, ya fara tsawata masa.
33 Amma da Yesu ya juya ya dubi almajiransa, sai ya tsawata wa Bitrus ya ce, “Tashi
daga nan Shaiɗan! Ba ka da al’amuran Allah a zuciyarka, sai na mutane.”
34 Sai ya kira taron wurinsa tare da almajiransa ya ce, “Duk wanda zai bi ni, dole
yă ƙi kansa, yă ɗauki gicciyensa yă bi ni. 35 Domin duk mai son ceton ransa zai rasa
shi, amma duk wanda ya rasa ransa saboda ni, da kuma bishara, zai same shi. 36 Me
mutum zai amfana, in ya ribato duniya duka a bakin ransa? 37 Ko kuma, me mutum
zai bayar a musayar ransa? 38 Duk wanda ya ji kunyata, da na kalmomina a wannan
zamani na fasikanci da zunubi, Ɗan Mutum ma zai ji kunyarsa lokacin da ya shiga
cikin ɗaukakar Ubansa, tare da tsarkakan mala’iku.”

## 9

1 Ya kuma ce musu, “Gaskiya nake gaya muku, waɗansu da suke tsattsaye a nan
ba za su mutu ba, sai sun ga mulkin Allah ya bayyana da iko.”

* **8:26** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da Kada ka faɗa wa kowa a ƙauyen † **8:29** Ko kuwa Almasihu “Kiristi” (da Girik) “Almasihu” kuma (da Ibraniyanci) duk suna nufin “Shafaffen nan.”

### *Sāke kamannin Yesu*
### *(Mattiyu 17.1-13; Luka 9.28-36)*

2 Bayan kwana shida, sai Yesu ya ɗauki Bitrus, Yaƙub da Yohanna tare da shi, ya
kai su kan wani dutse mai tsawo, suka kasance su kaɗai a wurin. A can aka sāke
kamanninsa a gabansu. 3 Tufafinsa suka zama fari suna ƙyalli, fiye da yadda wani a
duniya zai iya yi su. 4 Iliya da Musa suka bayyana a gabansu, suna magana da Yesu.
5 Bitrus ya ce wa Yesu, “Rabbi, ya yi kyau da muke nan. Bari mu kafa bukkoki guda
uku, ɗaya dominka, ɗaya domin Musa, ɗaya kuma domin Iliya.” 6 (Bai san abin da
zai faɗa ba ne, gama sun tsorata ƙwarai.)
7 Sai wani girgije ya bayyana, ya rufe su, wata murya kuma ta fito daga girgijen, ta
ce, “Wannan Ɗana ne, wanda nake ƙauna, ku saurare shi!”
8 Farat ɗaya, da suka waiwaya, ba su ƙara ganin kowa tare da su ba, sai dai Yesu.
9 Da suna saukowa daga dutsen, Yesu ya umarce su kada su gaya wa kowa abin da
suka gani, sai bayan Ɗan Mutum ya tashi daga matattu. 10 Suka riƙe wannan zance
a ɓoye tsakaninsu, suna tattaunawa ko mece ce ma’anar “tashi daga matattu.”
11 Suka tambaye shi, suka ce, “Don me malaman dokoki suke cewa, sai Iliya ya fara
zuwa?”
12 Yesu ya amsa ya ce, “Gaskiya ne, Iliya zai zo da fari, yă kuma mayar da dukan
abubuwa. Don me kuma aka rubuta cewa, dole Ɗan Mutum yă sha wahala sosai,
kuma a ƙi shi? 13 Amma ina faɗa muku, Iliya ya riga ya zo, kuma suka yi duk abin
da suka ga dama da shi, kamar yadda aka rubuta game da shi.”

### *Warkar da yaro mai mugun ruhu*
### *(Mattiyu 17.14-20; Luka 9.37-43)*

14 Da suka dawo wurin sauran almajiran, sai suka ga babban taro kewaye da su,
malaman dokoki suna gardama da su. 15 Nan take da dukan mutanen suka ga Yesu,
sai suka cika da mamaki, suka ruga da gudu don su gai da shi.
16 Ya tambaye su ya ce, “Gardamar me kuke yi da su?”
17 Wani mutum a cikin taron ya amsa ya ce, “Malam, na kawo maka ɗana mai
wani ruhun da yake hana shi magana. 18 Duk lokacin da mugun ruhun ya kama shi,
yakan jefa shi a ƙasa. Bakinsa yakan yi kumfa, yă cije haƙorarsa, yakan sa jikinsa
ya sandare, yă zama da ƙarfi. Na roƙi almajiranka su fitar da ruhun, amma ba su
iya ba.”
19 Yesu ya ce, “Ya ku zamani marar bangaskiya, har yaushe zan kasance tare da
ku? Har yaushe zan yi haƙuri da ku? Kawo mini yaron.”
20 Sai suka kawo shi. Da ruhun ya ga Yesu, nan da nan sai ya buge yaron da
farfaɗiya. Ya fāɗi a ƙasa, yana birgima, bakinsa yana kumfa.
21 Yesu ya tambayi mahaifin yaron ya ce, “Tun yaushe yake haka?”
Ya ce, “Tun yana ƙarami. 22 Ya sha jefa shi cikin wuta, ko ruwa don yă kashe shi.
Amma in za ka iya yin wani abu, ka ji tausayinmu ka taimake mu.”
23 Yesu ya ce, “ ‘In za ka iya’? Ai, kome mai yiwuwa ne ga wanda ya gaskata.”
24 Nan da nan mahaifin yaron ya faɗa da ƙarfi ya ce, “Na gaskata, ka taimake ni in
sha kan rashin bangaskiyata!”
25 Da Yesu ya ga taron suna zuwa can a guje, sai ya tsawata wa mugun ruhun ya
ce, “Kai ruhun kurma, da na bebe, na umarce ka, ka fita daga cikinsa, kada kuma ka
ƙara shigarsa.”
26 Sai ruhun ya yi ihu, ya buge shi da ƙarfi da farfaɗiya, ya fita. Yaron ya kwanta
kamar matacce, har mutane da yawa suka ce, “Ai, ya mutu.” 27 Amma Yesu ya kama
shi a hannu ya ɗaga, ya kuwa tashi tsaye.
28 Da Yesu ya shiga gida, almajiransa suka tambaye shi a ɓoye, suka ce, “Me ya sa
ba mu iya fitar da shi ba?”

29 Ya amsa ya ce, “Sai da addu’a[*]kaɗai irin wannan yakan fita.”
30 Suka bar wurin suka bi ta Galili. Yesu bai so wani yǎ san inda suke ba, 31 gama
yana koya wa almajiransa. Ya ce musu, “Za a ci amanar Ɗan Mutum, a ba da shi ga
hannun mutane. Za su kashe shi, bayan kwana uku kuma zai tashi.” 32 Amma ba su
fahimci abin da yake nufi ba, suka kuma ji tsoro su tambaye shi game da wannan.

### *Wane ne mafi girma?*
*(Mattiyu 18.1-5; Luka 9.46-48)*

33 Suka iso Kafarnahum. Da yana cikin gida, sai ya tambaye su ya ce, “Gardamar
me kuke yi a hanya?” 34 Amma suka yi shiru, don a hanya suna gardama ne, a kan
ko wane ne a cikinsu ya fi girma?
35 Da Yesu ya zauna, sai ya kira Sha Biyun ya ce, “In wani yana so yǎ zama na fari,
dole yǎ zama na ƙarshe duka, da kuma bawan kowa.”
36 Ya ɗauki wani ƙaramin yaro ya sa yǎ tsaya a tsakiyarsu. Ya ɗauke shi a hannunsa,
ya ce musu, 37 “Duk wanda ya karɓi ɗaya daga cikin waɗannan ƙananan yara a cikin
sunana, ni ya karɓa. Duk wanda kuma ya karɓe ni, ba ni ya karɓa ba, amma wanda
ya aiko ni ne ya karɓa.”

### *Wanda ba ya gāba da mu, namu ne*
*(Luka 9.49,50)*

38 Yohanna ya ce, “Malam mun ga wani mutum yana fitar da aljanu a cikin sunanka,
sai muka ce yǎ daina, domin shi ba ɗaya daga cikinmu ba ne.”
39 Yesu ya ce, “Kada ku hana shi. Ba wanda yake yin ayyukan banmamaki a cikin
sunana, nan take yǎ faɗi wani abu mummuna game da ni. 40 Gama duk wanda ba
ya gāba da mu, namu ne. 41 Gaskiya nake gaya muku, duk wanda ya ba ku ruwan
sha a sunana, saboda ku na Kiristi ne, lalle, ba zai rasa ladarsa ba.

### *Sanadin yin zunubi*
*(Mattiyu 18.6-9; Luka 17.1,2)*

42 “Idan kuma wani yǎ sa ɗaya daga cikin waɗannan ’yan yara masu gaskatawa
da ni yǎ yi laifi, zai fiye masa a rataya wani babban dutsen niƙa a wuyarsa, a jefa shi
cikin teku. 43 In hannunka yana sa ka yin zunubi, yanke shi. Ai, gwamma ka shiga
rai da hannu ɗaya, da ka shiga jahannama ta wuta, inda ba a iya kashe wutar ba, da
hannuwanka biyu.[†] 45 In kuma ƙafarka tana sa ka yin zunubi, yanke ta. Ai, gwamma
ka shiga rai da ƙafa ɗaya, da a jefa ka cikin jahannama ta wuta, da ƙafafunka biyu.[‡]
47 In kuma idonka yana sa ka zunubi, ƙwaƙule shi. Ai, gwamma ka shiga mulkin
Allah da ido ɗaya, da a jefa ka cikin jahannama ta wuta, da idanu biyu, 48 inda
“ ‘tsutsotsinsu ba sa mutuwa,
wutar kuma ba a iya kashewa.’[§]
49 Za a tsarkake kowa da wuta.
50 “Gishiri yana da daɗi, amma in ya rabu da ɗanɗanonsa, ta yaya za a sāke mai
da ɗanɗanonsa? Ku kasance da gishiri a cikinku, ku kuma yi zauna lafiya da juna.”

# 10

### *Kashen aure*
*(Mattiyu 19.1-12; Luka 16.18)*

1 Sai Yesu ya tashi daga nan ya tafi yankin Yahudiya, da kuma ƙetaren Urdun.
Taron mutane suka sāke zuwa wurinsa, ya kuma koya musu kamar yadda ya saba.

[*] **9:29** Waɗansu rubuce-rubucen hannu suna da addu’a da azumi [†] **9:43** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da fita, 44 inda “tsutsotsi masu cinsu ba sa mutuwa, wutar kuma ba a kashe ta.” [‡] **9:45** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da lahira, 46 inda “tsutsotsi masu cinsu ba sa mutuwa, wutar kuma ba a kashe ta.” [§] **9:48** Ish 66.24

2 Waɗansu Farisiyawa suka zo suka gwada shi, ta wurin yin masa tambaya cewa,
"Daidai ne bisa ga doka, mutum yă saki matarsa?"
3 Ya amsa ya ce, "Me Musa ya umarce ku?"
4 Suka ce, "Musa ya ba da izini mutum yă rubuta takardar saki, yă kuma kore ta."
5 Yesu ya ce, "Saboda taurin kanku ne, Musa ya rubuta muku wannan doka. 6 Amma
a farkon halitta, Allah ya 'halicce su miji da mace.'[*] 7 'Saboda wannan dalili, mutum
zai bar mahaifinsa da mahaifiyarsa, yă manne wa matarsa, 8 su biyun kuma za su
zama jiki ɗaya.'[†]Saboda haka, su ba mutum biyu ba ne, amma mutum ɗaya. 9 Domin
haka, abin da Allah ya haɗa, kada mutum yă raba."
10 Da suna cikin gida kuma, sai almajiran suka tambayi Yesu game da wannan. 11 Ya
amsa ya ce, "Duk wanda ya saki matarsa, ya auri wata, yana da laifin aikata zina a
kan matar da ya saki. 12 In kuma ta saki mijinta ta auri wani, ta yi zina ke nan."

### *Yesu da ƙananan yara*
### *(Mattiyu 19.13-15; Luka 18.15-17)*

13 Mutane suka kawo ƙananan yara wurin Yesu don yă taɓa su, amma almajiran
suka kwaɓe su. 14 Da Yesu ya ga haka, sai ya yi fushi, ya ce musu, "Ku bar yara
ƙanana su zo wurina, kada ku hana su, gama mulkin Allah na irin waɗannan ne.
15 Gaskiya nake gaya muku, duk wanda bai karɓi mulkin Allah kamar ƙaramin yaro
ba, ba zai taɓa shiga mulkin ba." 16 Sai ya ɗauki yaran a hannuwansa, ya ɗibiya
musu hannuwansa, ya kuma albarkace su.

### *Saurayi mai arziki*
### *(Mattiyu 19.16-30; Luka 18.18-30)*

17 Da Yesu ya kama hanya, sai wani mutum ya ruga da gudu ya zo wajensa, ya
durƙusa a gabansa ya ce, "Malam nagari, me zan yi domin in gāji rai madawwami?"
18 Yesu ya amsa ya ce, "Don me kake ce da ni mai nagarta? Ai, ba wani nagari, sai
Allah kaɗai. 19 Ka san dokokin da suka ce, 'Kada ka yi kisankai, kada ka yi zina, kada
ka yi sata, kada ka ba da shaida ta ƙarya, kada ka cuci wani, ka girmama mahaifinka
da mahaifiyarka.'[‡]"
20 Mutumin ya ce, "Malam, ai, tun ina yaro na kiyaye duk waɗannan."
21 Yesu ya kalle shi da ƙauna ya ce, "Abu ɗaya ka rasa, ka tafi ka sayar da duk abin
da kake da shi, ka ba wa matalauta, za ka kuwa sami dukiya a sama. Sa'an nan ka
zo ka bi ni."
22 Da jin wannan, sai mutumin ya ɓata fuskarsa, ya tafi da baƙin ciki, gama yana
da arziki sosai.
23 Yesu ya dudduba, sai ya ce wa almajiransa, "Yana da wuya fa masu arziki su
shiga mulkin Allah!"
24 Almajiransa suka yi mamakin kalmominsa. Amma Yesu ya sāke ce musu,
"'Ya'yana, yana da wuya fa a shiga mulkin Allah! 25 Ya fi sauƙi raƙumi yă shiga
ta kafar allura, da mai arziki yă shiga mulkin Allah."
26 Almajiran suka yi mamaki ƙwarai, suka ce wa juna, "To, wa zai sami ceto ke
nan?"
27 Yesu ya kalle su ya ce, "Ga mutum kam, wannan ba mai yiwuwa ba ne, amma
ga Allah, wannan mai yiwuwa ne; dukan abubuwa masu yiwuwa ne ga Allah."
28 Bitrus ya ce, "Mun bar kome domin mu bi ka!"
29 Yesu ya amsa ya ce, "Gaskiya nake gaya muku, babu wanda zai bar gida, ko
'yan'uwa maza da mata, ko mahaifiya, ko mahaifi, ko 'ya'ya, ko gonaki saboda ni, da
kuma bishara, 30 sa'an nan yă kāsa samun ninkinsu ɗari a zamanin yanzu (na gidaje,
da 'yan'uwa mata, da 'yan'uwa maza, da uwaye, da 'ya'ya, da gonaki amma tare da

[*] **10:6** Far 1.27 [†] **10:8** Far 2.24 [‡] **10:19** Fit 20.12; M Sh 5.16-20

tsanani) a lahira kuma yă sami rai madawwami. 31 Amma da yawa da suke na farko,
za su zama na ƙarshe, na ƙarshe kuma, za su zama na farko."

### *Yesu ya sāke yin zancen mutuwarsa*
### *(Mattiyu 20.17-19; Luka 18.31-34)*

32 Suna haurawa a hanyarsu zuwa Urushalima ke nan, Yesu yana a gaba, almajiran
suna bin sa suna mamaki, waɗanda suke bi kuma suna ji tsoro. Ya sāke kai Sha
Biyun nan gefe, ya gaya musu abin da zai faru da shi. 33 Ya ce, "Za mu haura zuwa
Urushalima, za a bashe Ɗan Mutum, ga manyan firistoci da malaman dokoki. Za su
yi masa hukuncin kisa, a kuma ba da shi ga Al'ummai, 34 waɗanda za su yi masa
ba'a, su tofa masa miyau, su yi masa bulala, su kuma kashe shi. Bayan kwana uku
kuma yă tashi."

### *Roƙon Yaƙub da Yohanna*
### *(Mattiyu 20.20-28)*

35 Sai Yaƙub da Yohanna, 'ya'yan Zebedi maza suka zo wurinsa suka ce, "Malam,
muna so ka yi mana duk abin da muka roƙa."

36 Ya tambaye su ya ce, "Me kuke so in yi muku?"

37 Suka amsa suka ce, "Ka bar ɗayanmu yă zauna a damarka, ɗayan kuma a
hagunka, a cikin ɗaukakarka."

38 Yesu ya ce, "Ba ku san abin da kuke roƙo ba. Za ku iya shan kwaf da zan sha, ko
a yi muku baftisma da baftismar da aka yi mini?"

39 Suka ce, "Za mu iya."

Yesu ya ce musu, "Za ku sha kwaf da zan sha, a kuma yi muku baftisma da aka yi
mini, 40 amma zama a damana ko haguna, ba ni nake ba da izinin ba. Waɗannan
wurare na waɗanda aka riga aka shirya musu ne."

41 Da sauran goman suka ji wannan, sai suka yi fushi da Yaƙub da Yohanna. 42 Yesu
ya kira su ya ce musu, "Kun sani waɗanda aka san su da mulkin al'ummai sukan
nuna musu iko, hakimansu ma sukan gasa musu iko. 43 Ba haka ya kamata yă zama
da ku ba. A maimakon, duk wanda yake so yă zama babba a cikinku, dole yă zama
bawanku. 44 Duk wanda kuma yake so yă zama na farko, dole yă zama bawan kowa.
45 Gama ko Ɗan Mutum ma, bai zo domin a bauta masa ba, amma don yă yi bauta,
yă kuma ba da ransa fansa saboda mutane da yawa."

### *Bartimawus makaho ya sami gani*
### *(Mattiyu 20.29-34; Luka 18.35-43)*

46 Sai suka iso Yeriko. Sa'ad da Yesu da almajiransa tare da taro mai yawa suke
barin birnin, wani makaho da ake kira Bartimawus kuwa (wato, "ɗan Timawus"),
yana zaune a gefen hanya yana bara. 47 Da ya ji cewa Yesu Banazare ne, sai ya ɗaga
murya, yana cewa, "Yesu Ɗan Dawuda, ka yi mini jinƙai!"

48 Mutane da yawa suka kwaɓe shi, suka ce yă yi shiru, amma ya ƙara ɗaga murya
yana cewa, "Dan Dawuda, ka yi mini jinƙai!"

49 Yesu ya tsaya ya ce, "Ku kira shi."

Sai suka kira makahon suka ce, "Ka yi farin ciki! Tashi tsaye! Yana kiranka." 50 Ya
jefar da mayafinsa waje ɗaya, ya yi wuf, ya zo wurin Yesu.

51 Yesu ya tambaye shi ya ce, "Me kake so in yi maka?"

Makahon ya ce, "Rabbi, ina so in sami ganin gari."

52 Yesu ya ce, "Je ka, bangaskiyarka ta warkar da kai." Nan da nan, ya sami ganin
gari, ya kuma bi Yesu suka tafi.

# 11

*Shiga mai nasara*
*(Mattiyu 21.1-11; Luka 19.28-40; Yohanna 12.12-19)*

1 Sa'ad da suka yi kusa da Urushalima, suka zo Betfaji da Betani wajen Dutsen
Zaitun, sai Yesu ya aiki biyu daga cikin almajiransa, 2 ya ce musu, "Ku je ƙauyen da
yake gaba da ku, da shigarku, za ku tarar da wani ɗan jaki a daure a can, wanda ba
wanda ya taɓa hawa. Ku kunce shi ku kawo nan. 3 In wani ya tambaye ku, 'Don me
kuke yin haka?' Ku gaya masa cewa, 'Ubangiji yana bukatarsa, zai kuma dawo da
shi ba da jimawa ba.' "

4 Suka tafi, suka kuwa tarar da wani ɗan jaki a waje, a titi, daure a ƙofar gida. Suna
cikin kunce shi ke nan, 5 sai waɗansu mutane da suke tsattsaye a wurin suka ce musu,
"Me kuke yi da kuke kunce ɗan jakin nan?" 6 Suka amsa kamar yadda Yesu ya ce su
yi. Mutanen kuwa suka ƙyale su. 7 Da suka kawo shi wajen Yesu, sai suka shimfiɗa
rigunarsu a bayansa. Yesu kuwa ya hau ya zauna bisansa. 8 Mutane da yawa suka
shimfiɗa rigunarsu a kan hanya, waɗansu kuma suka baza rassan itatuwan da suka
sara daga gonaki. 9 Waɗanda suka yi gaba, da kuma waɗanda suke biye, duk suka
ɗaga murya, suna cewa,

"Hosanna!*"

"Mai albarka ne wanda yake zuwa a cikin sunan Ubangiji!"†

10 "Mai albarka ne mulkin nan mai zuwa na mahaifinmu Dawuda!"

"Hosanna a can cikin samaniya!"

11 Yesu ya shiga Urushalima ya kuma tafi filin haikali. Ya dudduba kome duka,
amma da yake yamma ta yi, sai ya tafi Betani tare da Sha Biyun.

*Yesu ya tsabtacce haikali*
*(Mattiyu 21.18,19)*

12 Kashegari, da suke barin Betani, Yesu kuwa ya ji yunwa. 13 Da ya hangi wani
itacen ɓaure mai ganye, sai ya je domin yă ga ko yana da 'ya'ya. Amma da ya kai
can, bai tarar da kome ba sai ganye, domin ba lokacin 'ya'yan ɓaure ba ne. 14 Sai ya
ce wa itacen, "Kada kowa yă ƙara cin 'ya'yanka." Almajiransa kuwa suka ji ya faɗi
haka.

*(Mattiyu 21.12-17; Luka 19.45-48; Yohanna 2.13-22)*

15 Da suka kai Urushalima, sai Yesu ya shiga filin haikalin, ya fara korar waɗanda
suke saya da sayarwa a can. Ya tutture tebur na masu musayar kuɗi, da kujerun
masu sayar da tattabaru, 16 ya kuma hana kowa yă ratsa da a filin haikali ɗauke da
kayan ciniki. 17 Da yake koya musu, sai ya ce, "Ashe, ba a rubuce yake ba cewa, 'Za
a kira gidana, gidan addu'a na dukan al'ummai ba'?‡Amma ga shi kun mai da shi
'kogon 'yan fashi.'§"

18 Manyan firistoci da malaman dokoki suka ji wannan, sai suka fara neman hanyar
da za su kashe shi, gama suna jin tsoronsa, saboda dukan taron suna mamakin
koyarwarsa.

19 Da yamma ta yi, sai Yesu da almajiransa suka* bar garin.

*Itacen ɓaure da ya yanƙwane*
*(Mattiyu 21.20-22)*

* **11:9** Wani faɗi ne na Ibraniyanci mai ma'ana "Ceto!" Wanda ya zama kalmar yabo; haka ma a aya 10 † **11:9** Zab 118.25; Zab 118.26 ‡ **11:17** Ish 56.7 § **11:17** Irm 7.11 * **11:19** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na farko-farko suna da ya

[20] Da safe, da suke wucewa, sai suka ga itacen ɓauren nan ya yanƙwane tun daga
saiwarsa. [21] Bitrus ya tuna, sai ya ce wa Yesu, "Rabbi, duba! Itacen ɓauren nan da
ka la'anta, ya yanƙwane!"
[22] Yesu ya amsa ya ce, "Ku gaskata da Allah. [23] Gaskiya nake gaya muku, in wani
ya ce wa dutsen nan, 'Je ka, ka fāɗa cikin teku,' bai kuwa yi shakka a zuciyarsa ba,
amma ya gaskata cewa, abin da ya faɗa zai faru, haka kuwa za a yi masa. [24] Saboda
haka, ina faɗa muku, duk abin da kuka roƙa cikin addu'a, ku gaskata kun riga kun
karɓa, zai kuwa zama naku. [25] A duk lokacin da kuke tsaye cikin addu'a, in kuna
riƙe da wani mutum a zuciyarku, ku gafarta masa, domin Ubanku da yake sama shi
ma yă gafarta muku zunubanku."†

*An tuhumi ikon Yesu*
*(Mattiyu 21.23-27; Luka 20.1-8)*

[27] Suka sāke dawowa cikin Urushalima. Da Yesu yana tafiya a filin haikali, sai
manyan firistoci, malaman dokoki da kuma dattawa suka zo wurinsa. [28] Suka
tambaye, shi suka ce, "Da wane iko kake yin waɗannan abubuwa? Wa kuma ya
ba ka ikon yin wannan?"
[29] Yesu ya ce, "Zan yi muku tambaya guda. Ku ba ni amsa, ni kuma zan gaya muku,
ko da wane iko nake yin waɗannan abubuwa. [30] Baftismar Yohanna, daga sama ce,
ko daga mutane? Ku faɗa mini!"
[31] Sai suka tattauna a junansu, suka ce, "In muka ce, 'Daga sama ne,' zai ce, 'To,
don me ba ku gaskata shi ba?' [32] In kuma muka ce, 'Daga wurin mutane ne'; suna
jin tsoron mutane, don kowa ya ɗauka cewa, Yohanna, annabi ne na gaskiya."
[33] Saboda haka, suka amsa wa Yesu suka ce, "Ba mu sani ba."
Yesu ya ce, "To, ni ma ba zan gaya muku ko da wane iko nake yin waɗannan
abubuwa ba."

# 12

*Misalin 'yan haya*
*(Mattiyu 21.33-46; Luka 20.9-19)*

[1] Sa'an nan ya fara yi musu magana da misalai ya ce, "Wani mutum ya shuka
gonar inabi. Ya kewaye ta da katanga, ya haƙa rami domin matsin inabin, ya kuma
gina ɗakin gadi. Sai ya ba wa waɗansu manoma hayar gonar inabin, sa'an nan ya
yi tafiya. [2] Da lokacin girbi ya yi, sai ya aiki wani bawa wajen 'yan hayan, don yă
karɓo masa 'ya'yan inabin daga wurinsu. [3] Amma suka kama shi, suka yi masa dūka,
suka kore shi hannun wofi. [4] Sai ya sāke aikan wani bawa wurinsu, amma suka bugi
wannan mutum a kai, suka wulaƙanta shi. [5] Har yanzu ya sāke aikan wani. Wannan
kuwa suka kashe. Ya aika waɗansu da yawa; suka bubbuge waɗansu, sauran kuwa
suka kashe.
[6] "Sauran mutum ɗaya da ya rage ya aika, ɗa, da yake ƙauna. Daga ƙarshe sai ya
aike shi, yana cewa, 'Za su girmama ɗana.'
[7] "Amma 'yan hayan suka ce wa juna, 'Aha! Wannan shi ne magājin. Ku zo mu
kashe shi, gādon kuma yă zama namu.' [8] Sai suka kama shi suka kashe, suka jefa shi
bayan gonar inabin.
[9] "To, me, mai gonar inabin zai yi ke nan? Zai zo yă karkashe dukan 'yan hayan
nan, ya kuma ba wa waɗansu gonar inabin. [10] Ba ku taɓa karanta wannan Nassi ba,
" 'Dutsen da magina suka ƙi,
shi ne kuwa ya zama dutsen kusurwan gini.
[11] Ubangiji ya yi wannan,

† **11:25** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da zunubai. 26 Amma idan ba kwa yafewa, Ubanku ma da yake sama, ba zai yafe muku zunubanku ba.

ya kuma yi kyau a idanunmu'?"*
12 Sai manyan Firistoci da malaman dokoki da shugabanni suka nemi hanyar da za
su kama shi, domin sun gane ya yi misalin a kansu ne. Amma suka ji tsoron taron,
saboda haka suka bar shi suka yi tafiyarsu.

### *Biyan haraji ga Kaisar*
### *(Mattiyu 22.15-22; Luka 20.20-26)*

13 Daga baya, sai suka tura waɗansu Farisiyawa da mutanen Hiridus zuwa wurin
Yesu, domin su sa masa tarko a cikin maganarsa. 14 Suka zo wurinsa suka ce, "Malam,
mun san kai mutum ne mai mutunci. Ba ka bin ra'ayin mutane, don ba ka nuna
bambanci. Amma kana koyar da hanyar Allah bisa ga gaskiya. Daidai ne a biya wa
Kaisar haraji, ko babu? 15 Mu biya ko kada mu biya?"
Amma Yesu ya san munafuncinsu, sai ya yi tambaya ya ce, "Don me kuke ƙoƙarin
sa mini tarko? Ku kawo mini dinari in ga." 16 Suka kawo masa kuɗin, sai ya tambaye,
su ya ce, "Hoton wane ne wannan? Kuma rubutun wane ne wannan?"
Suka ce, "Na Kaisar."
17 Sai Yesu ya ce musu, "Ku ba wa Kaisar abin da yake na Kaisar, ku ba wa Allah
kuma abin da yake na Allah."
Suka yi mamakinsa ƙwarai.

### *Aure a tashin matattu*
### *(Mattiyu 22.23-33; Luka 20.27-40)*

18 Sa'an nan Sadukiyawa da suke cewa, babu tashin matattu, suka zo masa da
tambaya. 19 Suka ce, "Malam, Musa ya rubuta mana cewa, in ɗan'uwan wani mutum
ya mutu, ya bar mata babu 'ya'ya, dole mutumin ya auri gwauruwar, yǎ kuma samo
wa ɗan'uwansa 'ya'ya. 20 To, an yi waɗansu 'yan'uwa guda bakwai. Na fari ya yi
aure, ya mutu babu 'ya'ya. 21 Na biyun ya auri gwauruwar, sai shi ma ya mutu, babu
'ya'ya. Haka kuma na ukun. 22 A gaskiya, ba ko ɗaya daga cikin bakwai ɗin da ya
bar 'ya'ya. Daga ƙarshe, macen ta mutu. 23 To, a tashin matattu, matar wa za tǎ
zama, don duk su bakwai nan sun aure ta?"
24 Yesu ya ce, "Ashe, ba a cikin kuskure kuke ba saboda rashin sanin Nassi, ko ikon
Allah? 25 Sa'ad da matattu suka tashi, ba za su yi aure ba, ba kuwa za a ba da su ga
aure ba. Za su zama kamar yadda mala'iku suke a cikin sama. 26 Game da tashin
matattu kuwa, ashe, ba ku karanta a cikin littafin Musa ba, game da labarin ɗan
kurmin nan mai cin wuta da Musa ya gani a jeji, yadda Allah ya yi magana da shi
ya ce, 'Ni ne Allah na Ibrahim, Allah na Ishaku da kuma Allah na Yaƙub'?† 27 Shi ba
Allah na matattu ba ne, shi Allah na masu rai ne. Kun yi mummunan kuskure!"

### *Dokar da ta fi girma duka*
### *(Mattiyu 22.23-33; Luka 20.27-40)*

28 Wani daga cikin malaman dokoki ya zo ya ji suna muhawwara. Da ya lura cewa
Yesu ya amsa musu daidai, sai ya tambaye shi ya ce, "A cikin dukan dokoki, wacce
ta fi girma duka?"
29 Yesu ya ce, "Wadda ta fi girma duka, ita ce wannan. 'Ku saurara, ya Isra'ila,
Ubangiji Allahnmu, Ubangiji ɗaya ne. 30 Ka ƙaunaci Ubangiji Allahnka da dukan
zuciyarka, da dukan ranka, da dukan hankalinka, da kuma dukan ƙarfinka.'‡ 31 Na
biyun ita ce, 'Ka ƙaunaci maƙwabcinka kamar kanka.'§Ba wata doka da ta fi
waɗannan."
32 Mutumin ya ce, "Malam, ka faɗi daidai. Daidai ne da ka ce, Allah ɗaya ne, babu
kuma wani sai shi. 33 Nuna ƙauna ga Allah da dukan zuciyarka, da dukan ganewarka,

* **12:11** Zab 118.22,23 † **12:26** Fit 3.6 ‡ **12:30** M Sh 6.4,5 § **12:31** Fir 19.18

da dukan ƙarfinka, da kuma nuna ƙauna ga maƙwabcinka kamar kanka, ya fi dukan hadayun ƙonawa da sadakoki."

34 Da Yesu ya ga ya amsa da hikima, sai ya ce masa, "Ba ka da nisa da mulkin Allah." Daga lokacin, ba wanda ya yi karambani yin masa wata tambaya.

*Kiristi ɗan wane ne?*
*(Mattiyu 22.41-46; Luka 20.41-44)*

35 Yayinda Yesu yake koyarwa a filin haikalin, sai ya yi tambaya ya ce, "Yaya
malaman dokoki suke cewa Kiristi ɗan Dawuda ne? 36 Dawuda da kansa ya yi magana
ta wurin Ruhu Mai Tsarki ya ce,
" 'Ubangiji ya ce wa Ubangijina,
"Zauna a hannun damana
sai na sa abokan gābanka
a ƙarƙashin sawunka." '*
37 Dawuda da kansa ya kira shi 'Ubangiji.' To, ta yaya zai zama ɗansa?"

Taro mai yawa suka saurare shi da murna.

*(Mattiyu 23.1-36; Luka 20.45-47)*

38 Sa'ad da Yesu yake koyarwa ya ce, "Ku lura da malaman dokoki. Sukan so yin
tafiya a manyan riguna, a kuma dinga gaishe su a wuraren kasuwanci. 39 Sukan
kuma nemi wuraren zama mafi daraja a majami'u, da kuma wuraren zaman manya
a bukukkuwa. 40 Suna ƙwace gidajen gwauraye, kuma don nuna iyawa, sukan yi
dogayen addu'o'i. Irin mutanen nan, za su sha hukunci mai tsanani sosai."

*Bayarwar gwauruwa*

41 Yesu ya zauna ɗaura da inda ake bayarwa, ya kuma dubi yadda taron suke sa
kuɗinsu a cikin ɗakunan ajiya haikali. Masu arziki da yawa suka zuba kuɗaɗe masu
yawa. 42 Amma wata matalauciya gwauruwa, ta zo ta saka anini biyu, da suka yi
daidai da rabin kobo.
43 Yesu ya kira almajiransa wurinsa ya ce, "Gaskiya nake gaya muku, abin da
matalauciya gwauruwan nan ta zuba cikin ɗakunan ajiya nan ya fi na sauran dukan.
44 Dukansu sun bayar ne daga cikin arzikinsu; ita kuwa, daga cikin talaucinta, ta ba
da kome, duk abin da take da shi na rayuwa."

# 13

*Alamun ƙarshen zamani*
*(Mattiyu 24.1,2; Luka 21.5,6)*

1 Da yake barin haikalin, sai ɗaya daga cikin almajiransa ya ce masa, "Malam! Dubi irin manya-manyan duwatsun nan! Ka ga irin gine-ginen nan masu kyau mana!"

2 Yesu ya amsa ya ce, "Ka ga dukan manyan gine-ginen nan? Ba wani dutse a nan, da za a bari kan wani da ba za a rushe ba."

*(Mattiyu 24.3-14; Luka 21.7-19)*

3 Da Yesu yana zaune a kan Dutsen Zaitun da yake ɗaura da haikali, sai Bitrus,
Yaƙub, Yohanna da kuma Andarawus, suka tambaye shi a ɓoye, suka ce, 4 "Ka gaya
mana, yaushe waɗannan abubuwa za su faru? Wace alama ce kuma za tă nuna cewa,
duk waɗannan suna dab da cikawa?"
5 Sai Yesu ya ce musu, "Ku lura fa kada wani yă ruɗe ku. 6 Da yawa za su zo a
cikin sunana, suna cewa, 'Ni ne shi.' Za su kuwa ruɗi mutane da yawa. 7 Sa'ad da
kuka ji labarun yaƙe-yaƙe da jita-jitar yaƙe-yaƙe, kada hankalinku yă tashi. Dole
irin waɗannan abubuwa su faru. Amma ƙarshen tukuna. 8 Al'umma za tă tasar wa
al'umma, mulki kuma yă tasar wa mulki. Za a yi girgizar ƙasa a wurare dabam-dabam, a kuma yi yunwa. Waɗannan dai mafarin azabar naƙuda.

* **12:36** Zab 110.1

9 “Dole ku yi zaman tsaro. Za a ba da ku ga hukuma, a kuma bulale ku a majami’u.
Saboda ni kuma, za ku tsaya a gaban gwamnoni da sarakuna, domin ku ba da shaida
a gabansu. 10 Dole sai an fara yin wa’azin bishara ga dukan al’ummai. 11 Sa’ad da
aka kama ku, aka kuma kai ku don a yi muku shari’a, kada ku damu da abin da za
ku faɗa. Sai dai ku faɗi abin da aka ba ku a lokacin. Gama ba ku kuke magana ba,
Ruhu Mai Tsarki ne.
12 “Ɗan’uwa zai ba da ɗan’uwa a kashe. Mahaifi zai ba da ɗansa. ’Ya’ya za su
tayar wa iyayensu, su kuma sa a kashe su. 13 Dukan mutane za su ƙi ku saboda ni,
amma wanda ya tsaya da ƙarfi har ƙarshe, zai sami ceto.

*(Mattiyu 24.15-21; Luka 21.20-24)*

14 “Sa’ad da kuka ga ‘abin ƙyama, mai kawo hallaka’*tsaye inda†bai kamata ba (mai
karatu ya gane), to, sai waɗanda suke a Yahudiya su gudu zuwa duwatsu. 15 Kada
wani da yake kan rufin gidansa yă sauka, ko yă shiga gida don yă ɗauki wani abu.
16 Kada wani da yake gona kuma yă koma don ɗaukar rigarsa. 17 Kaiton mata masu
ciki, da mata masu renon ’ya’ya a waɗancan kwanakin! 18 Ku yi addu’a, kada wannan
yă faru a lokacin sanyi. 19 Domin waɗancan kwanakin za su zama kwanaki na baƙin
ciki, waɗanda ba a taɓa yin irinsa ba tun farkon halitta, har yă zuwa yanzu, ba kuwa
za a sāke yin irinsa ba.
20 “Da ba don Ubangiji ya rage kwanakin nan ba, da ba wani da zai tsira. Amma
saboda zaɓaɓɓu waɗanda ya zaɓa, sai ya rage kwanakin. 21 A lokacin nan, in wani
ya ce muku, ‘Duba, ga Kiristi nan!’ Ko kuwa, ‘Duba, ga shi can!’ Kada ku gaskata.
22 Gama Kiristi masu yawa na ƙarya, da annabawan ƙarya za su firfito, su kuma
aikata manyan alamu da ayyukan banmamaki don su ruɗi har da zaɓaɓɓu ma in zai
yiwu. 23 Amma ku kula! Na dai gaya muku kome tun da wuri.

*(Mattiyu 24.29-31; Luka 21.25-28)*

24 “Amma waɗancan kwanaki, bayan baƙin azaban nan,
“ ‘rana za tă yi duhu,
wata kuma ba zai ba da haskensa ba;
25 taurari za su fāɗɗāɗo daga sararin sama.
Za a kuma girgiza manyan abubuwan da suke a sararin sama.’‡
26 “Sa’an nan, mutane za su ga Ɗan Mutum yana zuwa cikin gizagizai da iko,
da ɗaukaka mai girma. 27 Zai kuma aiko mala’ikunsa su tattaro zaɓaɓɓunsa daga
kusurwoyi huɗun nan, daga iyakar duniya har yă zuwa iyakar sama.

*(Mattiyu 24.32-35; Luka 21.29-33)*

28 “To, sai ku yi koyi da itacen ɓaure. Da zarar rassansa suka yi taushi, ganyayensa
kuma suka toho, kun san cewa damina ta yi kusa ke nan. 29 Haka ma, in kuka
ga waɗannan abubuwa suna faruwa, ku san cewa ya yi kusan zuwa, yana ma dab
da bakin ƙofa. 30 Gaskiya nake gaya muku, zamanin nan ba zai shuɗe ba sai duk
abubuwan nan sun faru. 31 Sama da ƙasa za su shuɗe, amma kalmomina ba za su
taɓa shuɗewa ba.

### *Ba a san rana ko sa’a ba*
*(Mattiyu 24.36-44)*

32 “Game da wannan rana ko sa’a kuwa, ba wanda ya sani, ko mala’ikun da suke
sama, ko Ɗan, sai Uban kaɗai. 33 Ku lura fa! Ku zauna a shirye! Don ba ku san
lokacin da shi zai zo ba. 34 Yana kama da mutumin da zai yi tafiya. Yakan bar
gidansa a hannun bayinsa, kowa da nasa aikin da aka sa shi, yă kuma ce wa wanda
yake gadin ƙofa, yă yi tsaro.

---

* **13:14** Dan 9.27; Dan 11.31; Dan 12.11 † **13:14** Ko kuwa shi; haka ma a aya 29 ‡ **13:25** Ish 13.10; Ish 34.4

35 “Saboda haka, sai ku zauna a shirye, domin ba ku san lokacin da maigidan zai
dawo ba, ko da yamma ne, ko da tsakar dare ne, ko lokacin da zakara na cara ne, ko
kuma da safe ne. 36 In ya zo kwaram, kada ka bari yă tarar da kai kana barci. 37 Abin
da na faɗa muku, na faɗa wa kowa. ‘Ku yi tsaro!’ ”

# 14

*An shafe Yesu a Betani*
*(Mattiyu 26.1-5; Luka 22.1,2; Yohanna 11.45-53)*

1 To, saura kwana biyu ne kaɗai a yi Bikin Ketarewa da Bikin Burodi Marar Yisti,
sai manyan firistoci da malaman dokoki, suka nemi wani dalili su kama Yesu a ɓoye,
su kashe. 2 Suka ce, “Ba a lokacin Biki ba, don kada mutane su yi tawaye.”

*(Mattiyu 26.6-13; Yohanna 12.1-8)*

3 Yayinda yake a Betani, a gidan wani mutumin da ake kira Siman Kuturu, yana cin
abinci, sai wata mace ta zo da wani ɗan tulu na turaren alabasta da aka yi da nardi
zalla, mai tsadan gaske. Ta fasa tulun, ta kuma zuba turaren a kansa.
4 Waɗansu daga cikin waɗanda suke wurin, suka ji haushi, suka ce wa juna, “Me
ya sa za a ɓata turaren nan haka? 5 Da an sayar da shi, ai, da an sami kuɗi fiye da
albashi* ma’aikaci na shekara guda, a ba wa matalauta. Sai suka tsawata mata da
zafi.”
6 Yesu ya ce, “Ku ƙyale ta mana. Don me kuke damunta? Ta yi abu mai kyau a
gare ni. 7 Matalauta dai suna tare da ku kullum, za ku kuma iya taimakonsu a duk
lokacin da kuke so. Amma ni ba zan kasance da ku kullum ba. 8 Ta yi abin da ta iya
yi. Ta zuba turare a jikina kafin lokaci, don shirin jana’izata. 9 Gaskiya nake gaya
muku, duk inda aka yi wa’azin bishara ko’ina a duniya, za a faɗi abin da ta yi, domin
tunawa da ita.”

*(Mattiyu 26.14-16; Luka 22.3-6)*

10 Sai Yahuda Iskariyot, ɗaya daga cikin Sha Biyun nan, ya je wajen manyan firistoci
don yă bashe Yesu a gare su. 11 Suka yi murna da jin haka, suka yi alkawari za su ba
shi kuɗi. Don haka, ya fara neman zarafi yă ba da shi.

*Abincin yamma na Ubangiji*
*(Mattiyu 26.17-25; Luka 22.7-14,21-23; Yohanna 13.21-30)*

12 A rana ta fari ta Bikin Burodi Marar Yisti, lokacin da akan yanka ɗan ragon
hadayar kafara, bisa ga al’ada ta tunawa da Bikin Ketarewa, sai almajiran Yesu suka
tambaye shi, suka ce, “Ina kake so mu je mu shirya maka wurin da za ka ci Bikin
Ketarewa?”
13 Sai ya aiki biyu daga cikin almajiransa ya ce, “Ku shiga cikin birni, za ku sadu
da wani ɗauke da tulun ruwa. Ku bi shi. 14 Gidan da ya shiga, ku gaya wa maigidan
cewa, ‘Malam yana tambaya, ina ɗakin baƙina, inda zan ci Bikin Ketarewa tare da
almajiraina?’ 15 Zai nuna muku wani babban ɗakin sama da aka shirya domin baƙi.
Ku yi mana shirin a can.”
16 Almajiran suka tafi, suka shiga cikin birnin, suka kuwa tarar da kome kamar
yadda Yesu ya faɗa musu. Sai suka shirya Bikin Ketarewa.
17 Da yamma ta yi, sai Yesu ya zo tare da Sha Biyun. 18 Yayinda suke cin abinci
a tebur, sai ya ce, “Gaskiya nake gaya muku, ɗaya daga cikinku zai bashe ni, wani
wanda yake ci tare da ni.”
19 Suka cika da baƙin ciki, da ɗaya-ɗaya suka ce masa, “Tabbatacce, ba ni ba ne,
ko?”

---

* **14:5** Girik fiye da dinari ɗari uku

20 Ya ce, "Daya daga cikin Sha Biyun ne, wanda yake ci tare da ni a kwano. 21 Ɗan
Mutum zai tafi kamar yadda yake a rubuce game da shi, amma kaiton mutumin da
ya bashe Ɗan Mutum! Zai fi masa, da ba a haife shi ba."

*(Mattiyu 26.26-30; Luka 22.14-23; 1 Korintiyawa 11.23-25)*

22 Yayinda suke cin abinci, sai Yesu ya ɗauki burodi, ya yi godiya, ya kakkarya, ya ba wa almajiransa, yana cewa, "Ku karɓa, wannan jikina ne."

23 Sai kuma ya ɗauki kwaf ruwan inabi, ya yi godiya, ya kuma miƙa musu, dukansu suka sha daga ciki.

24 Sai ya ce musu, "Wannan jinina ne na alkawari, wanda aka zubar da shi saboda
mutane da yawa. 25 Gaskiya nake gaya muku, 'Ba zan ƙara sha daga 'ya'yan inabi
ba, sai ranan nan, da zan sha shi sabo a mulkin Allah.' "

26 Da suka rera waƙa, sai suka fita, suka tafi Dutsen Zaitun.

### *Yesu ya yi magana a kan mūsun Bitrus*

*(Mattiyu 26.31-35; Luka 22.31-34; Yohanna 13.36-38)*

27 Yesu ya ce musu, "Dukanku za ku ja da baya ku bar ni, gama yana a rubuce cewa,

" 'Zan bugi makiyayin tumaki,
tumakin kuwa za su warwatse.'[†]

28 Amma bayan na tashi, zan sha gabanku zuwa Galili."

29 Bitrus ya ce, "Ko da duka sun ja da baya suka bar ka, ba zan bar ka ba."

30 Yesu ya ce, "Gaskiya nake faɗa maka, yau, tabbatacce, a daren nan, kafin zakara
yă yi cara sau biyu[‡]kai da kanka za ka yi mūsun sanina sau uku."

31 Amma Bitrus ya yi ta nanatawa da ƙarfi ya ce, "Ko da zan mutu tare da kai, ba zan taɓa yin mūsun saninka ba." Duk sauran ma suka ce haka.

### *Getsemane*

*(Mattiyu 26.36-46; Luka 22.39-46)*

32 Suka tafi wani wurin da ake kira Getsemane, Yesu ya kuma ce wa almajiransa,
"Ku zauna a nan, yayinda ni kuwa in yi addu'a." 33 Ya tafi tare da Bitrus, Yaƙub da
kuma Yohanna. Sai ya fara baƙin ciki da damuwa ƙwarai. 34 Sai ya ce musu, "Raina
yana cike da baƙin ciki har ma kamar zan mutu. Ku dakata a nan ku yi tsaro."

35 Sai ya yi gaba kaɗan, ya fāɗi a ƙasa, ya yi addu'a, ya ce in mai yiwuwa ne, a
ɗauke masa wannan sa'a. 36 Ya ce, "Ya *Abba,*[§]Uba, kome mai yiwuwa ne a gare ka.
Ka ɗauke mini wannan kwaf. Amma ba abin da nake so ba, sai dai abin da kake so."

37 Sai ya koma wajen almajiransa, ya same su suna barci. Ya ce wa Bitrus, "Siman,
kana barci ne? Ka kāsa yin tsaro na sa'a ɗaya? 38 Ku yi tsaro, ku kuma yi addu'a,
domin kada ku fāɗi cikin jarraba. Ruhu yana so, sai dai jiki raunana ne."

39 Ya sāke komawa, ya maimaita addu'ar da ya yi. 40 Da ya dawo, ya sāke tarar da
su suna barci, domin barci ya cika musu ido. Suka rasa abin da za su ce masa.

41 Da ya koma sau na uku, sai ya ce musu, "Har yanzu kuna barci, kuna hutawa
ba? Ya isa! Lokaci ya yi. Duba an ba da Ɗan Mutum a hannun masu zunubi. 42 Ku
tashi! Mu tafi! Ga mai bashe ni ɗin yana zuwa!"

### *An kama Yesu*

*(Mattiyu 26.47-56; Luka 22.47-53; Yohanna 18.3-12)*

43 Yana cikin magana ke nan, sai Yahuda, ɗaya daga cikin Sha Biyun ya bayyana. Ya zo tare da taro da suke riƙe da takuba da sanduna. Manyan firistoci da malaman dokoki, da kuma dattawa ne suka turo taron.

---

† **14:27** Zak 13.7 ‡ **14:30** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na farko-farko ba su da sau biyu. § **14:36** Da Arameyik na Baba

44 Mai bashe shi ɗin ya riga ya shirya alama da su cewa, “Wanda na yi wa sumba,
shi ne mutumin, ku kama shi, ku riƙe sosai.” 45 Nan da nan Yahuda ya je wurin Yesu
ya ce, “Rabbi!” Ya kuma yi masa sumba. 46 Mutanen kuwa suka kama Yesu, suka
riƙe shi. 47 Sai wani cikin waɗanda suke tsattsaye kusa ya zāre takobinsa, ya sare
kunnen bawan babban firist.
48 Yesu ya ce, “Ina jagoran wani tawaye ne da kuka fito da takuba da kuma sanduna
domin ku kama ni? 49 Kowace rana ina tare da ku, ina koyarwa a filin haikali, ba ku
kama ni ba. Amma dole a cika Nassi.” 50 Sai kowa ya yashe shi ya gudu.
51 Wani saurayin da ba ya sanye da kome sai rigar lilin, yana bin Yesu. Da suka yi
ƙoƙarin kama shi, 52 sai ya gudu ya bar rigarsa, ya gudu tsirara.

### *A gaban majalisa*
*(Mattiyu 26.57-68; Luka 22.54,55,63-71; Yohanna 18.13,14,19-24)*

53 Suka kai Yesu wajen babban firist, sai dukan manyan firistoci, dattawa da kuma
malaman dokoki suka taru. 54 Bitrus ya bi shi daga nesa, har cikin filin gidan babban
firist. A can, ya zauna tare da masu gadi, yana jin ɗumin wuta.
55 Manyan firistoci da dukan ’yan Majalisa, suka shiga neman shaidar laifin da za
a tabbatar a kan Yesu, domin su kashe shi. Amma ba su sami ko ɗaya ba. 56 Da yawa
suka ba da shaidar ƙarya a kansa, amma shaidarsu ba tă zo ɗaya ba.
57 Sai waɗansu suka miƙe tsaye, suka ba da wannan shaida ƙarya a kansa, suka
ce, 58 “Mun ji shi ya ce, ‘Zan rushe wannan haikali da mutum ya gina, cikin kwana
uku, in sāke gina wani wanda ba ginin mutum ba.’ ” 59 Duk da haka ma, shaidarsu
ba tă zo ɗaya ba.
60 Sai babban firist ya tashi a gabansu, ya tambayi Yesu ya ce, “Ba za ka amsa ba?
Wane shaida ke nan waɗannan mutane suke kawowa a kanka?” 61 Amma Yesu ya yi
shiru, bai kuwa amsa ba.
Babban firist ya sāke tambayarsa ya ce, “Kai ne Kiristi, Ɗan Mai Albarka?”
62 Yesu ya ce, “Ni ne. Za ku kuwa ga Ɗan Mutum yana zaune a hannun dama na
Mai Iko, yana kuma zuwa a cikin gizagizan sama.”
63 Babban firist ya yage tufafinsa, ya yi ce, “Ina dalilin neman waɗansu shaidu
kuma? 64 Kun dai ji saɓon. Me kuka gani?”
Duka suka yanke masa hukuncin kisa. 65 Sai waɗansu suka fara tattofa masa miyau,
suka rufe masa idanu, suka bubbuge shi da hannuwansu, suka ce, “Yi annabci!” Masu
gadin kuma suka ɗauke shi, suka yi masa duka.

### *Bitrus ya yi mūsun sanin Yesu*
*(Mattiyu 26.69-75; Luka 22.56-62; Yohanna 18.15-18,25-27)*

66 Yayinda Bitrus yake ƙasa a filin gidan, sai wata yarinya, baiwa, ɗaya daga cikin
ma’aikatan babban firist, ta zo can. 67 Da ta ga Bitrus yana jin ɗumi, sai ta dube shi
da kyau.
Ta ce, “Kai ma kana tare da Yesu, Banazare.”
68 Amma ya yi mūsu ya ce, “Ban san abin da kike magana ba, balle ma in fahimce
ki.” Sai ya fita zuwa zaure.*
69 Da baiwar ta gan shi a can, sai ta sāke gaya wa waɗanda suke tsattsaye a wurin,
ta ce, “Wannan mutum yana ɗaya daga cikinsu.” 70 Sai ya sāke yin musu.
Bayan ɗan lokaci kaɗan, sai waɗanda suke tsattsaye kusa suka ce wa Bitrus, “Lalle,
kana ɗaya daga cikinsu, gama kai mutumin Galili ne.”
71 Sai ya fara la’antar kansa, yana rantsuwa musu, yana cewa, “Ban san wannan
mutumin da kuke magana a kai ba.”

---
* **14:68** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na farko-farko suna da ƙofar shiga zakara kuwa ya yi cara

72 Nan da nan zakara ya yi cara sau na biyu.† Sai Bitrus ya tuna da maganar da
Yesu ya yi masa cewa, "Kafin zakara yă yi cara sau biyu,‡za ka yi mūsun sanina sau
uku." Sai ya fashe da kuka.

# 15

### *Yesu a gaban Bilatus*
*(Mattiyu 27.1,2,11-14; Luka 23.1-5; Yohanna 18.28-38)*

1 Da sassafe, sai manyan firistoci da dattawa, da malaman dokoki, da dukan
Majalisa, suka yanke shawara. Suka daure Yesu, suka kai shi, suka miƙa shi ga Bilatus.
2 Bilatus ya yi tambaya ya ce, "Kai ne Sarkin Yahudawa?"
Yesu ya amsa ya ce, "I, haka yake, kamar yadda ka faɗa."
3 Manyan firistoci suka zarge shi a kan abubuwa da yawa. 4 Don haka Bilatus ya
sāke tambayarsa ya ce, "Ba za ka amsa ba? Dubi abubuwa da yawa da suke zarginka
da su."
5 Amma har yanzu, Yesu bai ba da amsa ba, Bilatus ya yi mamaki.
*(Mattiyu 27.15-26; Luka 23.13-25; Yohanna 18.39–19.16)*
6 Yanzu fa, al'ada ce a lokacin Bikin, a saki ɗan kurkuku guda wanda mutane suka
roƙa. 7 Wani mutumin da ake kira Barabbas, yana a kurkuku, tare da waɗansu 'yan
tawaye da suka yi kisankai a lokacin wani hargitsi. 8 Taron suka matso, suka ce roƙi
Bilatus yă yi musu abin da ya saba yi.
9 Bilatus ya yi tambaya ya ce, "Kuna so in sakar muku Sarkin Yahudawa?" 10 Don ya
san saboda sonkai ne manyan firistoci suka ba da Yesu a gare shi. 11 Amma manyan
firistoci suka zuga taron su sa a saki Barabbas, a maimakon Yesu.
12 Bilatus ya tambaye su ya ce, "To, me zan yi da wanda kuke ce da shi, sarkin
Yahudawa?"
13 Suka yi ihu, suka ce, "A gicciye shi!"
14 Bilatus ya yi tambaya ya ce, "Don me? Wane laifi ya yi?"
Amma suka ƙara yin ihu suna cewa, "A gicciye shi!"
15 Don son yă faranta wa taron rai, sai Bilatus ya sakar musu Barabbas. Ya sa aka
yi wa Yesu bulala, sa'an nan ya ba da shi a gicciye.

### *Sojoji sun yi wa Yesu ba'a*
*(Mattiyu 27.27-30; Yohanna 19.2,3)*

16 Sojojin suka tafi da Yesu cikin fadar gwamna (wato, Firetoriyum), suka kira dukan
kamfanin sojoji wuri ɗaya. 17 Suka sa masa wata riga mai ruwan shunayya, suka
kuma tuƙa rawanin ƙaya suka sa masa. 18 Sai suka fara ce masa, "Ranka yă daɗe
sarkin Yahudawa!" 19 Suka dinga bugunsa a kā da sanda, suka tattofa masa miyau.
Suka durƙusa suka yi masa bangirma na ba'a. 20 Bayan da suka gama yin masa ba'a,
suka tuɓe rigar mai ruwan shunayyar, suka sa masa nasa tufafi. Sai suka tafi da shi
don a gicciye shi.

### *Gicciyewa*
*(Mattiyu 27.27-30; Yohanna 19.2,3)*

21 Sai ga wani mutum daga Sairin da ake kira Siman, mahaifin Alekzanda da Rufus,
yana wucewa kan hanyarsa daga ƙauye. Sai suka tilasta shi yă ɗauki gicciyen. 22 Suka
kawo Yesu a wurin da ake kira Golgota (wanda yake nufin Wurin Koƙon Kai). 23 Sai
suka miƙa masa ruwan inabi gauraye da mur, don yă rage zafi, amma bai sha ba.
24 Sai suka gicciye shi. Suka rarraba tufafinsa, suka jefa ƙuri'a a kansu don su ga
abin da kowa zai samu.

---

† **14:72** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na farko-farko ba su da sau na biyu. ‡ **14:72** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na farko-farko ba su da sau biyu.

25 Saʼa ta uku na safe ce kuwa aka gicciye shi. 26 Akwai rubutu na zarginsa, da ya
ce,

Sarkin Yahudawa.

27 Suka gicciye ʼyan fashi biyu tare da shi, ɗaya a damansa, ɗayan kuma a hagunsa.*
29 Masu wucewa suka zazzage shi. Suka kaɗa kai suna cewa, “To, kai da za ka rushe
haikali ka kuma gina shi a kwana uku, 30 sai ka sauko daga gicciyen, ka ceci kanka!”
31 Haka kuma, manyan firistoci da malaman dokoki suka yi masa baʼa a junansu,
suna cewa, “Ya ceci waɗansu, amma ya kāsa ceton kansa! 32 Bari wannan Kiristi,
wannan Sarkin Israʼila, yǎ sauko yanzu daga gicciye, don mu ga mu kuma gaskata.”
Waɗanda aka gicciye tare da shi ma suka zazzage shi.

### *Mutuwar Yesu*
### *(Mattiyu 27.45-56; Luka 23.44-49; Yohanna 19.28-30)*

33 Daga saʼa ta shida har zuwa saʼa ta tara na rana, duhu ya rufe dukan ƙasar. 34 A
daidai saʼa ta tara na rana, sai Yesu ya ɗaga murya da ƙarfi ya ce, *“Eloi, Eloi, lama
sabaktani?”* (Wato, “Ya Allahna, ya Allahna, don me ka yashe ni?”).†
35 Da waɗansu cikin waɗanda suke tsattsaye kusa da wurin suka ji haka, suka ce,
“Ku saurara, yana kiran Iliya.”
36 Wani mutum ya ruga ya je ya jiƙo soso da ruwan tsami, ya soka a sanda ya miƙa
wa Yesu yǎ sha. Ya ce, “Ku ƙyale shi. Bari mu ga ko Iliya zai zo yǎ saukar da shi.”
37 Da murya mai ƙarfi, Yesu ya ja numfashinsa na ƙarshe.
38 Labulen haikali kuwa ya yage kashi biyu, daga sama har ƙasa. 39 Da jarumin
da yake tsaye a gaban Yesu ya ji muryarsa, ya kuma ga yadda ya mutu, sai ya ce,
“Gaskiya, wannan mutum Ɗan Allah ne!”
40 Waɗansu mata suna kallo daga nesa. A cikinsu kuwa akwai Maryamu Magdalin,
Maryamu mahaifiyar Yaƙub ƙarami da Yusuf,‡ da kuma Salome. 41 A Galili waɗannan
mata ne suka riƙa bin sa suna yin masa hidima. Waɗansu mata da yawa da suka zo
tare da shi daga Urushalima, su ma suna nan a can.

### *Janaʼizar Yesu*
### *(Mattiyu 27.57-61; Luka 23.50-56; Yohanna 19.38-42)*

42 Ranar kuwa ita ce ranar Shirye-shirye (wato, ana kashegari Asabbaci). Saboda
haka, da yamma ta yi, sai 43 Yusuf daga Arimateya, wani sanannen ɗan Majalisa,
wanda dā ma yake jiran zuwan mulkin Allah, ya je wajen Bilatus ba tsoro, ya roƙa
a ba shi jikin Yesu. 44 Bilatus ya yi mamaki da ya ji cewa Yesu ya riga ya mutu. Sai
ya kira jarumin ya tambaye shi ko Yesu ya riga ya mutu. 45 Da ya ji ta bakin jarumin
cewa haka ne, sai ya ba wa Yusuf jikin. 46 Sai Yusuf ya kawo zanen lilin, ya saukar
da jikin, ya nannaɗe shi da lilin ɗin, saʼan nan ya sa shi a kabarin da aka fafe a cikin
dutse. Sai ya gungura wani dutse ya rufe bakin kabarin. 47 Maryamu Magdalin da
Maryamu uwar Yusuf sun ga inda aka kwantar da shi.

# 16

### *Tashin Yesu daga matattu*
### *(Mattiyu 28.1-8; Luka 24.1-12; Yohanna 20.1-10)*

1 Da Asabbaci ya wuce, sai Maryamu Magdalin, Maryamu mahaifiyar Yaƙub, da
kuma Salome suka sayi kayan ƙanshi domin su je su shafa wa jikin Yesu. 2 A ranar
farko ta mako, da sassafe, bayan fitowar rana, suna kan hanyarsu zuwa kabarin ke

---

* **15:27** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da hagu, 28 Nassin nan kuwa ya cika da ya ce, “An lasafta shi a cikin masu laifi.” (Ish 53.12) † **15:34** Zab 22.1 ‡ **15:40** Girik Yosi, wani sunan Yusuf; haka ma a aya 47

nan, 3 sai suka tambaye juna suka ce, “Wane ne zai gungura mana dutsen daga bakin
kabarin?”
4 Amma da suka ɗaga kai, sai suka ga cewa, an riga an gungura dutsen. Dutsen
kuwa babba ne. 5 Da suna shiga cikin kabarin, sai suka ga wani saurayi sanye da
farar riga, yana zaune a hannun dama, sai suka firgita.
6 Ya ce, “Kada ku firgita. Kuna neman Yesu Banazare wanda aka gicciye ne. Ya
tashi! Ba ya nan. Ku dubi inda aka kwantar da shi. 7 Amma ku tafi ku gaya wa
almajiransa da kuma Bitrus cewa, ‘Ya sha gabanku zuwa Galili. Can za ku gan shi,
kamar yadda ya faɗa muku.’ ”
8 Da rawan jiki da kuma ruɗewa, matan suka fita a guje daga kabarin. Ba su kuwa
gaya wa kowa ba, don suna tsoro.

[Waɗansu rubuce-rubucen hannu na farko-farko da waɗansu shaidu na dā ba su da ayoyi 9-20.]

9 *Da Yesu ya tashi daga matattu da safe, a ranar farko ta mako, ya fara bayyana ga*
*Maryamu Magdalin, wadda ya fitar da aljanu bakwai daga cikinta.* 10 *Ta je ta gaya wa*
*waɗanda dā suke tare da shi, waɗanda kuma suke makoki da kuka.* 11 *Da suka ji cewa*
*Yesu yana da rai, har ma ta gan shi, ba su gaskata ba.*

*(Luka 24.13-35)*

12 *Daga baya Yesu ya bayyana a wani kamanni dabam ga biyunsu, yayinda suke*
*tafiya ƙauye.* 13 *Waɗannan kuwa suka koma suka shaida wa sauran, amma su ma ba*
*su gaskata ba.*
14 *Bayan haka, Yesu ya bayyana ga Sha Ɗayan, yayinda suke cin abinci. Ya tsawata*
*musu a kan rashin bangaskiyarsu, da yadda suka ƙi gaskata waɗanda suka gan shi*
*bayan ya tashi.*
15 *Ya ce, musu, “Ku tafi cikin dukan duniya, ku yi wa’azin bishara ga dukan halitta.*
16 *Duk wanda ya gaskata, aka kuma yi masa baftisma, zai sami ceto. Amma duk*
*wanda bai gaskata ba kuwa, zai hallaka.* 17 *Waɗannan alamu za su kasance tare*
*da waɗanda suka gaskata. A cikin sunana za su fitar da aljanu, za su yi magana da*
*sababbin harsuna.* 18 *Za su ɗauki macizai da hannuwansu. In kuwa suka sha mugun*
*dafi, ba zai cuce su ba ko kaɗan. Za su ɗibiya hannuwansu a kan marasa lafiya, su*
*kuwa warke.”*
19 *Bayan Ubangiji Yesu ya yi musu magana, sai aka ɗauke shi zuwa sama, ya kuma*
*zauna a hannun dama na Allah.* 20 *Sai almajiran suka fita, suka yi wa’azi ko’ina.*
*Ubangiji kuwa ya yi aiki tare da su, ya tabbatar da maganarsa ta wurin alamu da suke*
*biye da maganar.*

# Luka

*Gabatarwa*

1 Mutane da yawa sun ɗau niyyar rubuta labarin abubuwan da aka cika a cikinmu,
2 kamar yadda muka karɓe su daga waɗanda tun farko shaidu ne da kuma masu
hidimar bishara. 3 Saboda haka, da yake ni da kaina na binciko kome a hankali daga
farko, na ga ya yi kyau in rubuta maka labarin dalla-dalla, ya mafifici Tiyofilus, 4 don
ka san tabbacin abubuwan da aka koyar da kai.

*An yi faɗar haihuwar Yohanna Mai Baftisma*

5 A lokacin da Hiridus ne yake sarautar Yahudiya, an yi wani firist mai suna
Zakariya, na sashin firistoci gidan Abiya. Matarsa Elizabet ma ʼyar zuriyar Haruna
ce. 6 Dukansu biyu kuwa masu adalci ne a gaban Allah, suna kuma bin umarnan
Ubangiji da farillansa duka da halin rashin zargi. 7 Sai dai ba su da ʼyaʼya, domin
Elizabet bakararriya ce; kuma dukansu biyu sun tsufa.

8 Wata rana da lokacin aikin firistoci na sashen Zakariya na yin hidima ya kewayo,
yana kuma cikin hidimarsa ta firist a gaban Allah, 9 sai aka zaɓe shi ta wurin ƙuriʼa,
bisa ga alʼadar aikin firist, yă shiga haikalin Ubangiji yă ƙone turare. 10 Da lokacin
ƙone turare ya yi, duk taron masu sujada suna a waje suna adduʼa.

11 Sai malaʼikan Ubangiji ya bayyana gare shi, tsaye a dama da bagaden turare.
12 Da Zakariya ya gan shi sai ya firgita, tsoro kuma ya kama shi. 13 Amma malaʼikan
ya ce masa, “Kada ka ji tsoro, Zakariya; an ji adduʼarka. Matarka Elizabet za tă haifa
maka ɗa, za ka kuma ba shi suna Yohanna. 14 Zai zama abin murna da farin ciki a
gare ka, mutane da yawa kuwa za su yi murna don haihuwarsa, 15 gama zai zama
mai girma a gaban Ubangiji. Ba kuwa zai taɓa shan ruwan inabi ko wani abu mai sa
maye ba. Zai cika da Ruhu Mai Tsarki tun haihuwa. 16 Shi ne zai juye mutanen Israʼila
da yawa zuwa wurin Ubangiji Allahnsu. 17 Zai sha gaban Ubangiji, a ruhu da kuma
iko irin na Iliya, domin yă juye zukatan iyaye ga ʼyaʼyansu, marasa biyayya kuma ga
zama masu biyayya don yă kintsa mutane su zama shiryayyu domin Ubangiji.”

18 Sai Zakariya ya tambayi malaʼikan ya ce, “Yaya zan tabbatar da wannan? Ga ni
tsoho, matana kuma ta kwana biyu.”

19 Malaʼikan ya ce, “Ni ne Jibraʼilu. Ina tsaya a gaban Allah, an kuma aiko ni in
yi maka magana, in kuma faɗa maka wannan labari mai daɗi. 20 Yanzu za ka zama
bebe, ba za ka ƙara iya magana ba sai ranar da wannan magana ta cika, saboda ba
ka gaskata da kalmomina waɗanda za su zama gaskiya a daidai lokacinsu ba.”

21 Ana cikin haka, mutane suna jiran Zakariya, suna kuma mamaki me ya sa ya
daɗe haka a cikin haikali. 22 Da ya fito, bai iya yin musu magana ba. Sai suka
gane, ya ga wahayi ne a haikali, domin ya dinga yin musu alamu, amma ya kāsa yin
magana.

23 Da lokacin hidimarsa ya cika, sai ya koma gida. 24 Bayan wannan, matarsa
Elizabet ta yi ciki, ta kuma riƙa ɓuya har wata biyar. 25 Sai ta ce, “Ubangiji ne ya yi
mini wannan. A waɗannan kwanaki ya nuna tagomashinsa ya kuma kawar mini da
kunya a cikin mutane.”

*Annabcin haihuwar Yesu*

26 A wata na shida, sai Allah ya aiki malaʼika Jibraʼilu zuwa Nazaret, wani gari a
Galili, 27 gun wata budurwar da aka yi alkawarin aurenta ga wani mutum mai suna
Yusuf daga zuriyar Dawuda. Sunan budurwar Maryamu. 28 Malaʼikan ya je wurinta
ya ce, “A gaishe ki, ya ke da kika sami tagomashi ƙwarai! Ubangiji yana tare da ke.”

29 Maryamu ta damu ƙwarai da kalmominsa, tana tunani wace irin gaisuwa ce
haka? 30 Amma mala'ikan ya ce mata, “Kada ki ji tsoro, Maryamu, kin sami tagomashi
a wurin Allah. 31 Ga shi za ki yi ciki ki kuma haifi ɗa, za ki kuma ba shi suna Yesu.
32 Zai zama mai girma, za a kuma kira shi Ɗan Maɗaukaki. Ubangiji Allah zai ba shi
gadon sarautar kakansa Dawuda, 33 zai yi mulkin gidan Yaƙub har abada, mulkinsa
kuma ba zai taɓa ƙare ba.”
34 Maryamu ta tambayi mala'ikan ta ce, “Yaya wannan zai yiwu, da yake ni
budurwa ce?”
35 Mala'ikan ya amsa ya ce, “Ruhu Mai Tsarki zai sauko miki, ikon Maɗaukaki kuma
zai rufe ke. Saboda haka, Mai Tsarkin nan da za a haifa, za a kira shi* Ɗan Allah.
36 'Yar'uwarki Elizabet ma za tă haifi ɗa a tsufanta, ita da aka ce bakararriya, ga shi
tana a watanta na shida. 37 Gama ba abin da zai gagari Allah.”
38 Maryamu ta amsa ta ce, “To, ni baiwar Allah ce, bari yă zama mini kamar yadda
ka faɗa.” Sai mala'ikan ya tafi abinsa.

### *Maryamu ta ziyarci Elizabet*

39 A lokacin sai Maryamu ta shirya ta gaggauta zuwa wani gari a ƙasar tudu ta
Yahudiya, 40 inda ta shiga gidan Zakariya ta kuma gai da Elizabet. 41 Da Elizabet
ta ji gaisuwar Maryamu, sai jaririn da yake a cikinta ya yi motsi. Elizabet kuma ta
cika da Ruhu Mai Tsarki. 42 Sai ta ɗaga murya da ƙarfi ta ce, “Ke mai albarka ce a
cikin mata. Mai albarka ne kuma ɗan da za ki haifa! 43 Me ya sa na sami wannan
tagomashi har da mahaifiyar Ubangijina za tă zo wurina? 44 Da jin gaisuwarki, sai
jaririn da yake cikina ya yi motsi don murna. 45 Mai albarka ce wadda ta gaskata
cewa abin da Ubangiji ya faɗa mata zai cika!”

### *Waƙar Maryamu*

46 Sai Maryamu ta ce,
“Raina yana ɗaukaka Ubangiji
47 ruhuna kuma yana farin ciki da Allah Mai Cetona,
48 gama ya lura da ƙasƙancin baiwarsa.
Daga yanzu nan gaba dukan zamanai za su ce da ni mai albarka,
49 gama Mai Iko Duka ya yi mini manyan abubuwa,
sunansa labudda Mai Tsarki ne.
50 Jinƙansa ya kai ga masu tsoronsa,
daga zamani zuwa zamani.
51 Ya aikata manyan ayyuka da hannunsa;
ya watsar da waɗanda suke masu girman kai a zurfin tunaninsu.
52 Ya saukar da masu mulki daga gadajen sarautarsu
amma ya ɗaukaka ƙasƙantattu.
53 Ya ƙosar da masu yunwa da kyawawan abubuwa
amma ya sallami mawadata hannu wofi.
54 Ya taimaki bawansa Isra'ila,
yana tunawa yă nuna jinƙai
55 ga Ibrahim da zuriyarsa har abada,
kamar yadda ya faɗa wa kakanninmu.”
56 Maryamu ta zauna da Elizabet kusan wata uku sa'an nan ta koma gida.

### *Haihuwar Yohanna Mai Baftisma*

* **1:35** Ko kuwa Saboda haka, yaron da za a haifa za a kira shi mai tsarki

57 Sa’ad da kwanaki suka yi don Elizabet ta haihu, sai ta haifi ɗa. 58 Maƙwabtanta
da ’yan’uwanta suka ji cewa Ubangiji ya nuna mata jinƙai mai yawa, suka kuma taya
ta farin ciki.
59 A rana ta takwas, sai suka zo don a yi wa yaron kaciya, dā za su sa masa
sunan mahaifinsa Zakariya ne, 60 amma mahaifiyar yaron ta ce, “A’a! Za a ce da
shi Yohanna.”
61 Sai suka ce mata, “Ba wani a cikin danginku mai wannan suna.”
62 Sai suka yi alamu wa mahaifinsa, don su san sunan da zai su a kira yaron. 63 Ya
yi alama a kawo masa allo, a gaban kowa sai ya rubuta, “Sunansa Yohanna.” Dukan
mutane kuwa suka yi mamaki. 64 Nan da nan bakinsa ya buɗe harshensa kuma ya
saku, sai ya fara magana yana yabon Allah. 65 Maƙwabta duk suka cika da tsoro,
mutane kuwa suka yi ta yin magana game da dukan waɗannan abubuwa a ko’ina a
cikin ƙasar tudu ta Yahudiya. 66 Duk waɗanda suka ji wannan kuwa sun yi mamaki
suna cewa, “To, me yaron nan zai zama?” Gama hannun Ubangiji yana tare da shi.

### *Waƙar Zakariya*

67 Mahaifinsa Zakariya ya cika da Ruhu Mai Tsarki sai ya yi annabci ya ce,

68 “Yabo ya tabbata ga Ubangiji, Allah na Isra’ila,
domin ya zo ya kuma fanshe mutanensa.
69 Ya tā mana ƙahon ceto
a gidan bawansa Dawuda
70 (yadda ya yi magana tun tuni ta wurin annabawansa masu tsarki),
71 cewa zai cece mu daga abokan gābanmu
daga kuma hannun dukan waɗanda suke ƙinmu
72 don yă nuna jinƙai ga kakanninmu,
yă kuma tuna da alkawarinsa mai tsarki,
73 rantsuwar da ya yi wa mahaifinmu Ibrahim,
74 don yă kuɓutar da mu daga hannun abokan gābanmu,
yă kuma sa mu iya yin masa hidima babu tsoro,
75 cikin tsarki da adalci a gabansa dukan kwanakinmu.

76 “Kai kuma, ɗana, za a ce da kai annabin Maɗaukaki;
gama za ka sha gaban Ubangiji don ka shirya masa hanya,
77 don ka sanar da mutanensa ceto,
ta wurin gafarar zunubansu,
78 saboda jinƙai na Allahnmu mai ƙauna,
hasken nan na ceto zai ɓullo mana daga sama,
79 don yă haskaka a kan waɗanda suke zama cikin duhu,
da kuma cikin inuwar mutuwa,
don yă bi da ƙafafunmu a hanyar salama.”

80 Yaron kuwa ya yi girma ya kuma ƙarfafa a ruhu; ya zauna a hamada sai lokacin
da ya fito a fili ga mutanen Isra’ila.

# 2

### *Haihuwar Yesu*
### *(Mattiyu 1.18-25)*

1 A waɗancan kwanaki, Kaisar Augustus ya ba da doka cewa ya kamata a yi ƙidaya
a dukan masarautar Roma. 2 (Wannan ce ƙidaya ta fari da aka yi a lokacin da
Kwiriniyus yake gwamnar Suriya.) 3 Sai kowa ya koma garinsa don a rubuta shi.

4 Saboda haka Yusuf ma ya haura daga Nazaret a Galili zuwa Yahudiya, ya tafi
Betlehem garin Dawuda, don shi daga gida da kuma zuriyar Dawuda ne. 5 Ya tafi can
don a rubuta shi tare da Maryamu, wadda aka yi masa alkawari zai aura, tana kuwa
da ciki. 6 Yayinda suke can, sai lokacin haihuwar jaririn ya yi, 7 ta kuwa haifi ɗanta
na fari. Ta nannaɗe shi a zane ta kuma kwantar da shi cikin wani kwami, don ba su
sami ɗaki a masauƙi ba.

### *Makiyaya da Mala'iku*

8 Akwai makiyaya masu zama a fili kusa da wurin, suna tsaron garkunan tumakinsu
da dare. 9 Sai wani mala'ikan Ubangiji ya bayyana gare su, ɗaukakar Ubangiji kuma
ta haskaka kewaye da su, suka kuwa tsorata ƙwarai. 10 Amma mala'ikan ya ce musu,
"Kada ku ji tsoro. Na kawo muku labari mai daɗi na farin ciki mai yawa ne wanda
zai zama domin dukan mutane. 11 Yau a birnin Dawuda an haifa muku Mai Ceto;
shi ne Kiristi Ubangiji. 12 Wannan zai zama alama a gare ku. Za ku tarar da jariri a
nannaɗe a zane kwance a kwami."

13 Ba labari sai ga taron rundunar sama suka bayyana tare da mala'ikan, suna
yabon Allah suna cewa,

14 "Daukaka ga Allah a can cikin sama,
a duniya kuma salama ga mutane waɗanda tagomashinsa yake bisansu."

15 Da mala'ikun suka bar su, su suka koma sama, sai makiyayan suka ce wa juna,
"Mu je Betlehem mu ga wannan abin da ya faru, wanda Ubangiji ya sanar mana."

16 Sai suka tafi da sauri, suka tarar da Maryamu da Yusuf, da kuma jaririn kwance
a kwami. 17 Sa'ad da suka gan shi, sai suka baza maganar da aka gaya musu game
da yaron, 18 duk kuwa waɗanda suka ji wannan, suka yi mamaki a kan abin da
makiyayan suka faɗa. 19 Amma Maryamu ta riƙe dukan waɗannan abubuwa ta
kuma yi ta tunaninsu a zuciyarta. 20 Makiyayan kuwa suka koma, suna ɗaukaka
suna kuma yabon Allah saboda dukan abubuwan da suka ji, suka kuma gani, yadda
aka gaya musu.

### *Miƙa Yesu a haikali*

21 A rana ta takwas, da lokaci ya yi da za a yi masa kaciya, sai aka ba shi suna Yesu,
sunan da mala'ika ya ba shi kafin a yi cikinsa.

22 Da lokacin tsarkakewarsu bisa ga Dokar Musa ya cika, sai Yusuf da Maryamu
suka ɗauke shi suka haura zuwa Urushalima don su miƙa shi ga Ubangiji 23 (yadda
yake a rubuce a Dokar Ubangiji cewa, "Kowane ɗan fari, za a keɓe shi ga Ubangiji"*),
24 don kuma su miƙa hadaya bisa ga abin da aka faɗa a Dokar Ubangiji cewa,
"kurciyoyi biyu ko 'yan tattabarai biyu."†

25 To, akwai wani mutum a Urushalima mai suna Siman, shi mai adalci da kuma
mai ibada. Yana jiran fansar Isra'ila, Ruhu Mai Tsarki kuwa yana tare da shi. 26 An
bayyana masa ta wurin Ruhu Mai Tsarki cewa ba zai mutu ba sai ya ga Kiristi na
Ubangiji. 27 Da Ruhu ya iza shi, sai ya shiga cikin filin haikali. Sa'ad da iyayen suka
kawo jaririn nan Yesu don su yi masa abin da al'adar Doka ta bukaci, 28 sai Siman ya
karɓi yaron a hannuwansa ya yabi Allah, yana cewa,

29 "Ya Ubangiji Mai Iko Duka, kamar yadda ka yi alkawari,
yanzu ka sallami bawanka lafiya.
30 Gama idanuna sun ga cetonka,
31 wanda ka shirya a gaban dukan mutane,
32 haske don bayyanawa ga Al'ummai
da kuma ɗaukaka ga mutanenka Isra'ila."

---

* **2:23** Fit 13.2,12 † **2:24** Fir 12.8

33 Mahaifin yaron da kuma mahaifiyarsa suka yi mamaki abin da aka faɗa game
da shi. 34 Sa'an nan Siman ya sa musu albarka ya ce wa Maryamu mahaifiyarsa, "An
ƙaddara yaron nan yă zama sanadin fāɗuwa da tashin mutane da yawa a Isra'ila, zai
kuma zama alamar da mutane ba za su so ba, 35 ta haka za a fallasa tunanin zukatan
mutane da yawa. Ke ma, takobi zai soki zuciyarki."
36 Akwai wata annabiya ma, mai suna Anna, diyar Fanuwel, na kabilar Asher. Ta
tsufa kutuf; ta yi zama da mijinta shekaru bakwai bayan sun yi aure, 37 ta kuwa zama
gwauruwa sai da ta kai shekaru tamanin da huɗu.‡ Ba ta taɓa barin haikali ba, tana
sujada dare da rana, tana kuma azumi da addu'a. 38 Tana haurawa wurinsu ke nan
a wannan lokaci, sai ta yi wa Allah godiya ta kuma yi magana game da yaron nan ga
dukan waɗanda suke sauraron fansar Urushalima.
39 Bayan da Yusuf da Maryamu suka gama yin dukan abubuwan da Dokar Ubangiji
ta bukaci, sai suka koma Galili suka tafi Nazaret garinsu. 40 Yaron kuwa ya yi girma
ya yi ƙarfi; ya cika da hikima, alherin Allah kuwa yana bisansa.

### *Yesu a haikali*

41 Kowace shekara, iyayen Yesu sukan je Urushalima don Bikin Ketarewa. 42 Da
Yesu ya cika shekaru goma sha biyu, sai suka tafi Bikin bisa ga al'ada. 43 Bayan
Bikin, da iyayen suka kama hanya don su koma gida, sai Yesu, yaron nan, ya
tsaya a Urushalima, ba da saninsu ba. 44 Su kuwa sun ɗauka yana tare da su,
saboda haka, suka yi ta tafiya har na yini guda. Sa'an nan suka fara nemansa
cikin 'yan'uwansu da abokansu. 45 Da ba su gan shi ba, sai suka koma Urushalima
nemansa. 46 Bayan kwana uku, sai suka same shi a filin haikali zaune a tsakiyar
malamai, yana sauraronsu yana kuma yi musu tambayoyi. 47 Dukan waɗanda suka
ji shi, suka yi mamakin fahimtarsa, da amsoshinsa. 48 Da iyayensa suka gan shi sai
suka yi mamaki. Mahaifiyarsa ta ce masa, "Dana, don me ka yi mana haka? Ni da
mahaifinka duk mun damu muna nemanka."
49 Sai ya ce, "Don me kuke nemana? Ba ku san cewa, dole in kasance a gidan Ubana
ba?" 50 Amma ba su fahimci abin da yake faɗin musu ba.
51 Sai ya koma Nazaret tare da su, yana yi musu biyayya. Mahaifiyarsa kuma ta
riƙe dukan waɗannan abubuwa a zuciyarta. 52 Yesu kuwa ya yi girma, ya kuma ƙaru
cikin hikima, ya kuma sami tagomashi a wurin Allah da mutane.

# 3

### *Yohanna Mai Baftisma ya shirya hanya*
### *(Mattiyu 3.1-12; Markus 1.1-8; Yohanna 1.19-28)*

1 A shekara ta goma sha biyar ta mulkin Kaisar Tiberiyus, a lokacin Buntus Bilatus
ne gwamnar Yahudiya, Hiridus kuma yana sarautar Galili, ɗan'uwansa Filibus yana
sarautar Ituriya da Tarakunitis, Lisaniyas kuma yana sarautar Abiline. 2 A lokacin ne
Annas da Kayifas suke manyan firistoci. Sai maganar Allah ta zo wa Yohanna, ɗan
Zakariya a hamada. 3 Ya zaga dukan ƙasar da take kewaye da Urdun, yana wa'azin
baftismar tuba don gafarar zunubai. 4 Kamar yadda yake a rubuce a littafin annabi
Ishaya.

"Muryar mai kira a hamada,
'Ku shirya wa Ubangiji hanya,
ku miƙe hanyoyi dominsa.
5 Za a cike kowane kwari,
a farfashe kowane dutse da kowane tudu.
Za a miƙe hanyoyin da suka karkace,
a gyaggyara hanyoyi masu gargaɗa su zama sumul.

‡ **2:37** Ko kuwa gwauruwa na shekaru tamanin da huɗu.

6 Dukan ʼyan Adam kuwa za su ga ceton Allah!ʼ ”*
7 Yohanna ya ce wa taron da suke zuwa domin yă yi musu baftisma, “Ku macizai!
Wa ya gargaɗe ku, ku guje wa fushin nan mai zuwa? 8 Ku yi ayyukan da suka dace
da tuba. Kada ma ku yi tunani za ku iya ce wa kanku, ‘Ai, muna da mahaifinmu
Ibrahim.’ Ina gaya muku cewa daga cikin duwatsun nan Allah zai iya tā da ʼyaʼya
wa Ibrahim. 9 An riga an sa bakin gatari a gindin itatuwa, kuma duk itacen da bai
ba da ʼyaʼya masu kyau ba, za a sare shi a jefa cikin wuta.”
10 Sai taron suka tambaye shi, suka ce “Me za mu yi ke nan?”
11 Ya amsa ya ce, “Ya kamata, mutumin da yake da riguna biyu, yă raba da wanda
ba shi da riga, mai abinci kuma yă yi haka.”
12 Masu karɓar haraji ma suka zo, domin a yi musu baftisma. Suka yi tambaya,
suka ce “Malam, me ya kamata mu yi?”
13 Ya ce musu, “Kada ku karɓa fiye da abin da aka ce a karɓa.”
14 Sai waɗansu sojoji suka tambaye shi, “Mu fa? Me ya kamata mu yi?”
Sai ya amsa ya ce, “Kada ku ƙwace kuɗin mutane, kada kuma ku yi shaidar ƙarya.
Ku yi haƙuri da abin da ake biyanku.”
15 Mutane suka zuba ido, suna kuma tunani a zuciyarsu, ko Yohanna ne Kiristi
wanda ake sauraron zuwansa. 16 Yohanna ya amsa musu duka ya ce, “Ina muku
baftisma da ruwa. Amma wani wanda ya fi ni iko yana zuwa, ban ma isa in kunce
igiyar takalmansa ba. Shi zai yi muku baftisma da Ruhu Mai Tsarki da wuta kuma.
17 Matankaɗinsa yana a hannunsa don yă tankaɗe sussukarsa ya kuma tattara alkama
cikin rumbunsa, amma zai ƙone yayin da wutar da ba a iya kashewa.” 18 Da kalmomi
masu yawa Yohanna ya yi wa mutane gargaɗi, ya kuma yi musu waʼazin bishara.
19 Amma da Yohanna ya tsawata wa Hiridus mai mulki saboda Hiridiyas, matar
ɗanʼuwansa, da kuma dukan sauran mugayen abubuwan da ya yi, 20 Hiridus dai ya
ƙara ɓata alʼamarin. Ya sa a kulle Yohanna a kurkuku.

### *Baftismar Yesu da kuma asalinsa*
### *(Mattiyu 3.13-17; Markus 1.9-11)*

21 Saʼad da ake wa dukan mutane baftisma, sai aka yi wa Yesu shi ma. Da yana
cikin adduʼa, sai sama ya buɗe, 22 Ruhu Mai Tsarki kuma ya sauko masa a wata siffa,
kamar kurciya. Sai murya ta fito daga sama, ta ce, “Kai ne Ɗana, wanda nake ƙauna,
kai ne kuma kana faranta mini zuciya ƙwarai.”

### *(Mattiyu 1.1-17)*

23 To, Yesu kansa yana da shekaru kusan talatin da haihuwa saʼad da ya fara aikinsa.
An ɗauka shi ɗan Yusuf ne,

ɗan Heli, 24 ɗan Mattat,
ɗan Lawi, ɗan Melki,
ɗan Yannai, ɗan Yusuf,
25 ɗan Mattatiyas, ɗan Amos,
ɗan Nahum, ɗan Esli,
ɗan Naggai, 26 ɗan Maʼat,
ɗan Mattatiyas, ɗan Semeyin,
ɗan Yosek, ɗan Yoda,
27 ɗan Yowanan, ɗan Resa,
ɗan Zerubbabel, ɗan Sheyaltiyel,
ɗan Neri, 28 ɗan Melki,
ɗan Addi, ɗan Kosam,
ɗan Elmadam, ɗan Er,

---
* **3:6** Ish 40.3-5

29 ɗan Yoshuwa, ɗan Eliyezer,
ɗan Yorim, ɗan Mattat,
ɗan Lawi, 30 ɗan Simeyon,
ɗan Yahuda, ɗan Yusuf,
ɗan Yonam, ɗan Eliyakim,
31 ɗan Meleya, ɗan Menna,
ɗan Mattata, ɗan Natan,
ɗan Dawuda, 32 ɗan Yesse,
ɗan Obed, ɗan Bowaz,
ɗan Salmon,† ɗan Nashon,
33 ɗan Amminadab, ɗan Ram,‡
ɗan Hezron, ɗan Ferez,
ɗan Yahuda, 34 ɗan Yaƙub,
ɗan Ishaku, ɗan Ibrahim,
ɗan Tera, ɗan Nahor,
35 ɗan Serug, ɗan Reyu,
ɗan Feleg, ɗan Eber,
ɗan Sala, 36 ɗan Kainan,
ɗan Arfakshad, ɗan Shem,
ɗan Nuhu, ɗan Lamek,
37 ɗan Metusela, ɗan Enok,
ɗan Yared, ɗan Mahalalel,
ɗan Kainan, 38 ɗan Enosh,
ɗan Shitu, ɗan Adamu,
ɗan Allah.

# 4

*Gwajin Yesu*
*(Mattiyu 4.1-11; Markus 1.12,13)*

1 Yesu kuwa cike da Ruhu Mai Tsarki, ya dawo daga Urdun, Ruhu kuma ya kai
shi cikin hamada, 2 inda kwana arba'in, Iblis ya gwada shi. Bai ci kome ba a cikin
kwanakin nan, a ƙarshensu kuwa ya ji yunwa.
3 Iblis ya ce masa, "In kai Ɗan Allah ne, ka faɗa wa wannan dutse yǎ zama burodi."
4 Yesu ya amsa ya ce, "A rubuce yake, 'Ba da abinci kaɗai mutum zai rayu ba.'*"
5 Iblis ya kai shi can kan wani wuri mai tsawo, ya nunnuna masa a ƙyiftawar ido
dukan mulkokin duniya. 6 Ya ce masa, "Zan ba ka dukan ikonsu da darajarsu, gama
ni aka danƙa wa, kuma zan bai wa duk wanda na ga dama. 7 Saboda haka in ka yi
mini sujada, dukan wannan zai zama naka."
8 Yesu ya amsa ya ce, "A rubuce yake, 'Ka yi wa Ubangiji Allahnka sujada, kuma
shi kaɗai za ka bauta wa.'†"
9 Sai Iblis, ya kai shi Urushalima ya sa ya tsaya a kan wuri mafi tsayi na haikali ya
ce, "In kai Ɗan Allah ne, ka yi tsalle daga nan zuwa ƙasa. 10 Gama a rubuce yake,
" 'Zai umarci mala'ikunsa game da kai,
su kiyaye ka da kyau;
11 za su tallafe ka da hannuwansu,
don kada ka buga ƙafarka a kan dutse.'‡"
12 Yesu ya amsa ya ce, "An ce, 'Kada ka gwada Ubangiji Allahnka.'§"

† **3:32** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na farko-farko suna da Sala ‡ **3:33** Waɗansu rubuce-rubucen hannu suna Amminadab, ɗan Admin, ɗan Arni; waɗansu rubuce-rubucen hannun kuma sun bambanta sosai. * **4:4** M Sh 8.3 † **4:8** M Sh 6.13 ‡ **4:11** Zab 91.1,12 § **4:12** M Sh 6.16

13 Da Iblis ya gama dukan wannan gwajin, ya bar shi sai lokacin da wata dama ta
samu.

### *An ƙi Yesu a Nazaret*
*(Mattiyu 4.12-17; Markus 1.14,15)*

14 Yesu ya koma Galili cikin ikon Ruhu. Labarinsa kuwa ya bazu ko'ina a ƙauyuka.
15 Ya yi ta koyarwa a majami'unsu, kowa kuwa ya yabe shi.

*(Mattiyu 13.53-58; Markus 6.1-6)*

16 Ya tafi Nazaret, inda aka yi renonsa. A ranar Asabbaci kuma, ya shiga majami'a
kamar yadda ya saba. Sai ya miƙe don yǎ yi karatu. 17 Aka kuwa ba shi naɗaɗɗen
littafin annabi Ishaya. Da ya buɗe, sai ya sami wurin da aka rubuta,
18 "Ruhun Ubangiji yana kaina,
domin ya shafe ni,
in yi wa matalauta wa'azin bishara.
Ya aiko ni in yi shelar 'yanci ga 'yan kurkuku,
in kuma buɗe idanun makafi,
in ba da 'yanci ga waɗanda aka danne.
19 In yi shelar shekarar tagomashin Ubangiji."*
20 Sai ya naɗe naɗaɗɗen littafin ya mayar wa mai hidimar, ya kuma zauna. Dukan
idanun waɗanda suke a majami'ar, suka koma a kansa. 21 Sai ya fara ce musu, "A
yau, Nassin nan, ya cika a kunnenku."
22 Duk suka yabe shi, suka yi mamakin kalmomin alheri da suke fitowa daga
bakinsa. Suka yi tambaya, suna cewa, "Anya, wannan ba ɗan Yusuf ba ne?"
23 Yesu ya ce musu, "Tabbatacce, na san za ku faɗa mini karin maganan nan, 'Likita,
warkar da kanka! Ka kuma yi abin da muka ji ka yi a Kafarnahum, a nan garinka.' "
24 Ya ci gaba, da ce musu, "Gaskiya nake gaya muku, babu annabin da ake yarda
da shi a garinsa. 25 Ina tabbatar muku a zamanin Iliya, akwai gwauraye da yawa a
Isra'ila, sa'ad da aka rufe sararin sama har shekara uku da rabi, aka kuma yi yunwa
mai tsanani ko'ina a ƙasar. 26 Duk da haka, ba a aiki Iliya ga ko ɗaya a cikinsu
ba. Sai dai zuwa ga wata gwauruwa da take a Zarefat, a yankin Sidon. 27 Akwai
kuma mutane da yawa a Isra'ila masu kuturta a zamanin annabi Elisha, amma ba
ko ɗayansu da aka tsarkake sai Na'aman mutumin Suriyan nan kaɗai."
28 Dukan mutanen da suke cikin majami'a suka fusata ƙwarai da jin wannan.
29 Suka tashi, suka fitar da Yesu bayan gari, suka kai shi goshin tudun da aka gina
garin, don su ture shi ƙasa, 30 amma sai ya bi ta tsakiyar taron ya yi tafiyarsa.

### *Yesu ya fitar da mugun ruhu*
*(Markus 1.21-28)*

31 Sai ya tafi Kafarnahum, wani gari a Galili, a ranar Asabbaci kuma, ya fara koya
wa mutane. 32 Suka yi ta mamakin koyarwarsa, domin saƙonsa yana da iko.
33 A cikin majami'ar, akwai wani mutum mai aljani, wani mugun ruhu. Mutumin
ya ɗaga murya da ƙarfi ya ce, 34 "Wayyo! Ina ruwanka da mu, Yesu Banazare? Ka zo
ne don ka hallaka mu? Na san wane ne kai, Mai Tsarki na Allah!"
35 Yesu ya tsawata masa da ƙarfin cewa, "Yi shiru! Ka fita daga cikinsa!" Sai
aljanin ya fyaɗa mutumin da ƙasa a gabansu duka, sa'an nan ya fita, ya bar shi ba
wani rauni.
36 Dukan mutanen suka yi mamaki, suka ce wa junansu, "Wace irin koyarwa ce
haka? Da ƙarfi da iko, yana ba wa mugayen ruhohin umarni suna kuma fita!"
37 Labarinsa kuwa ya bazu ko'ina a cikin ƙasar.

---

* **4:19** Ish 61.1 2

### *Yesu ya warkar da mutane da yawa*
### *(Mattiyu 8.14-17; Markus 1.29-34)*

38 Yesu ya fita daga majami'ar, ya tafi gidan Siman. Surukar Siman kuwa tana fama
da zazzaɓi mai tsanani, sai suka roƙi Yesu yǎ taimake ta. 39 Sai ya sunkuya kusa da
ita, ya kuma tsawata wa zazzaɓin, sai zazzaɓin ya sāke ta. Nan take ta tashi, ta yi
musu hidima.
40 Rana tana fāɗuwa, sai mutane suka yi ta kawo wa Yesu dukan waɗanda suke da
cuta iri-iri, sai ya ɗibiya wa kowannensu hannuwansa, ya warkar da su. 41 Bugu da
ƙari, aljanu suka fiffita daga cikin mutane da yawa suna ihu suna cewa, "Kai Ɗan
Allah ne!" Amma ya kwaɓe su, ya hana su magana, don sun san cewa shi ne Kiristi.†
42 Da gari yana wayewa, sai Yesu ya je inda ba kowa. Mutane suka yi ta nemansa,
da suka zo inda yake, sai suka yi ƙoƙari su hana shi barinsu. 43 Amma ya ce, "Dole in
yi wa'azin bisharar mulkin Allah ga sauran garuruwa, saboda wannan ne aka aiko
ni." 44 Sai ya dinga yin wa'azi a majami'un Yahudiya.

# 5

### *Kiran almajirai na farko*
### *(Mattiyu 8.14-17; Markus 1.29-34)*

1 Wata rana, Yesu yana tsaye a bakin Tafkin Gennesaret, mutane kuma suna ta
matsawa kewaye da shi, domin su ji maganar Allah, 2 sai ya hangi jiragen ruwa biyu
a bakin tafkin, waɗanda masu kamun kifi suka bari suna wankin abin kamun kifinsu.
3 Sai ya shiga ɗaya jirgin ruwan da yake na Siman, ya kuma roƙe shi yǎ tura shi kaɗan
daga gaci. Sai ya zauna a jirgin ruwan, ya koyar da mutane daga ciki.
4 Da ya gama magana, sai ya ce wa Siman, "Ka tuƙa jirgin zuwa inda akwai zurfi,
ka saukar da abin kamun kifinka ka kama kifi."
5 Siman ya amsa ya ce, "Ranka yǎ daɗe, duk dare mun yi ta fama ba mu kama
kome ba, amma tun da ka ce haka, zan saki abin kamun kifin."
6 Da suka yi haka, sai suka kama kifi da yawa, har abin kamun kifinsu suka fara
tsintsinkewa. 7 Sai suka kira abokansu a ɗaya jirgin, su zo su taimake su, suka kuwa
zo. Suka cika jiragen biyu da kifi cif, har jiragen suka fara nutsewa.
8 Da Siman Bitrus ya ga wannan, sai ya fāɗi a gaban Yesu ya ce, "Rabu da ni,
Ubangiji. Ni mai zunubi ne!" 9 Gama mamaki ya kama shi da abokansa duka, saboda
yawan kifin da suka kama. 10 Yaƙub da Yohanna, 'ya'yan Zebedi, abokan aikin Siman
su ma suka yi mamaki.
Sai Yesu ya ce wa Siman, "Kada ka ji tsoro, daga yanzu za ka riƙa kama mutane
ne." 11 Sai suka jawo jiragen ruwansu zuwa gaci, suka bar kome da kome, suka bi
shi.

### *Warkar da kuturu*
### *(Mattiyu 8.1-4; Markus 1.40-45)*

12 Yayinda Yesu yake ɗaya daga cikin garuruwan nan, sai ga wani mutum wanda
kuturta ta ci ƙarfinsa. Da ganin Yesu, sai ya fāɗi da fuskarsa a ƙasa, ya roƙe shi ya
ce, "Ubangiji, in ka yarda, kana iya ka tsabtacce ni."
13 Yesu ya miƙa hannunsa ya taɓa mutumin ya ce, "Na yarda, ka zama da tsabta!"
Nan da nan, sai kuturtar ta rabu da shi.
14 Sai Yesu ya umarce shi ya ce, "Kada ka gaya wa kowa, amma ka tafi ka nuna
kanka ga firist, ka kuma miƙa hadayu da Musa ya umarta, saboda tsarkakewarka ta
zama shaida a gare su."

---

† **4:41** Ko kuwa Almasihu

15 Duk da haka, labarinsa ya ƙara bazuwa sosai, har taron mutane suka dinga zuwa
don jinsa, da kuma neman warkarwa daga cututtukansu. 16 Amma Yesu sau da yawa,
yakan keɓe kansa zuwa wuraren da ba kowa, yă yi addu'a.

### *Yesu ya warkar da shanyayye*
### *(Mattiyu 9.1-8; Markus 2.1-12)*

17 Wata rana, da yake cikin koyarwa, waɗansu Farisiyawa da malaman dokoki
waɗanda suka zo daga kowane ƙauye a Galili, Yahudiya da Urushalima kuwa suna
zaune. Ikon Ubangiji yana nan don yă warkar da masu ciwo. 18 Sai ga waɗansu
mutane suka kawo wani shanyayye a kan tabarma. Suka yi ƙoƙari su shigar da shi
cikin gidan, domin su kwantar da shi a gaban Yesu. 19 Da suka ga babu hanyar da
za su bi saboda taron, sai suka haura rufin, suka saukar da shi a kan tabarmarsa, ta
bakin ramin da suka huda a rufin, suka ajiye shi a tsakiyar taron, a gaban Yesu.
20 Da Yesu ya ga bangaskiyarsu, sai ya ce, "Saurayi, an gafarta maka zunubanka."
21 Farisiyawa da malaman dokoki suka fara yin tunani a zukatansu, "Wane ne
wannan mutum da yake saɓo haka? Wa zai iya gafarta zunubai, in ba Allah kaɗai
ba?"
22 Yesu ya san abin da suke tunani, sai ya yi tambaya ya ce, "Don me kuke tunanin
waɗannan abubuwa a zukatanku? 23 Wanne ya fi sauƙi, a ce, 'An gafarta maka
zunubanka,' ko kuma a ce, 'Tashi, ka yi tafiya'? 24 Amma domin ku san cewa Ɗan
Mutum yana da iko a duniya ya gafarta zunubai." Sai ya ce wa shanyayyen, "Na ce
maka, tashi, ɗauki tabarmarka ka tafi gida." 25 Nan da nan, ya tashi tsaye a gabansu,
ya ɗauki tabarmar da yake kwance a kai, ya tafi gida, yana yabon Allah. 26 Kowa ya
yi mamaki, ya kuma yabi Allah. Suka cika da tsoro, suna cewa, "Mun ga abubuwan
banmamaki yau."

### *Kiran Lawi*
### *(Mattiyu 9.9-13; Markus 2.13-17)*

27 Bayan wannan, sai Yesu ya fita, ya ga wani mai karɓar haraji, mai suna Lawi,
yana zaune a wurin da ake karɓar haraji. Yesu ya ce masa, "Bi ni." 28 Sai Lawi ya
tashi, ya bar kome da kome, ya bi shi.
29 Sai Lawi ya shirya wa Yesu wani babban liyafa a gidansa. Wani babban taron na
masu karɓar haraji, tare da waɗansu suna cin abinci tare da su. 30 Amma Farisiyawa
da malaman dokokin da suke a ƙungiyarsu, suka yi wa almajiransa gunaguni, suna
cewa, "Don me kuke ci, kuke sha tare da masu karɓar haraji da masu zunubi?"
31 Yesu ya amsa musu ya ce, "Ai, masu lafiya ba sa bukatar likita, sai dai marasa
lafiya. 32 Ban zo don in kira masu adalci ba, sai dai masu zunubi zuwa ga tuba."

### *An tuhumi Yesu a kan azumi*
### *(Mattiyu 9.14-17; Markus 2.18-22)*

33 Suka ce masa, "Almajiran Yohanna sukan yi azumi da addu'a, haka ma almajiran
Farisiyawa, amma naka sai ci da sha."
34 Yesu ya amsa ya ce, "Za ku iya sa abokan ango yin azumi yayinda yake tare
da su? 35 Amma lokaci yana zuwa, da za a ɗauke ango daga gare su. A waɗancan
kwanakin ne za su yi azumi."
36 Sai ya faɗa musu wannan misali ya ce, "Ba wanda yakan yage ƙyalle daga
sabuwar riga ya yi wa tsohuwar riga faci. In ya yi haka, zai yage sabuwar rigar,
kuma facin daga sabuwar ba zai dace da tsohuwar rigar ba. 37 Kuma ba wanda
yakan zuba sabon ruwan inabi a cikin tsofaffin salkuna. In ya yi haka, sabon ruwan
inabi zai farfashe salkunan, ruwan inabin yă zube, salkunan kuma su lalace. 38 A'a,
sai dai a zuba sabon ruwan inabi a sababbin salkuna. 39 Kuma ba wanda yakan so
shan sabon ruwan inabi bayan ya sha tsohon, don yakan ce, 'Ai, tsohon ya fi kyau.' "

# 6

*Ubangijin Asabbaci*
*(Mattiyu 12.1-8; Markus 2.23-28)*
1 A wata ranar Asabbaci, Yesu yana bi ta gonakin hatsi, sai almajiran suka fara
kakkarya kan hatsi suna murjewa a hannuwansu suna ci. 2 Sai waɗansu Farisiyawa
suka ce, "Me ya sa kuke yin abin da doka ta hana yi a ranar Asabbaci?"
3 Yesu ya amsa musu ya ce, "Ashe, ba ku taɓa karanta abin da Dawuda ya yi,
sa'ad da shi da abokan tafiyarsa suka ji yunwa ba? 4 Ya shiga gidan Allah, ya ɗauki
keɓaɓɓen burodi, sa'an nan ya ci abin da firistoci kaɗai sukan ci bisa ga doka. Ya
kuma ba wa abokan tafiyarsa?" 5 Sai Yesu ya ce musu, "Ai, Ɗan Mutum ne Ubangijin
Asabbaci."
*(Mattiyu 12.9-14; Markus 3.1-6)*
6 A wata ranar Asabbaci kuma, Yesu ya shiga majami'a yana koyarwa. To, a nan
kuwa akwai wani mutumin da hannun damansa ya shanye. 7 Farisiyawa da malaman
dokoki suka zuba wa Yesu ido, su ga ko zai warkar a ranar Asabbaci, don su sami
dalilin zarginsa. 8 Amma Yesu ya san abin da suke tunani. Sai ya ce wa mutumin mai
shanyayyen hannun, "Tashi ka tsaya a gaban kowa." Sai ya tashi ya tsaya.
9 Yesu ya ce musu, "Ina tambayarku, me ya kamata a yi bisa ga doka, a ranar
Asabbaci, a aikata alheri ko a aikata mugunta, a ceci rai, ko a hallaka shi?"
10 Sai ya kalle su duka, sa'an nan ya ce wa mutumin, "Miƙo hannunka." Sai ya
miƙe, hannunsa kuwa ya koma lafiyayye. 11 Amma Farisiyawa da malaman Doka
suka fusata, suka fara tattauna da junansu a kan abin da za su yi wa Yesu.

*Manzanni sha biyu*
*(Mattiyu 10.1-4; Markus 3.13-19)*
12 Wata rana, a cikin kwanakin nan, Yesu ya je wani dutse domin yǎ yi addu'a, ya
kuma kwana yana addu'a ga Allah. 13 Da gari ya waye, sai ya kira almajiransa zuwa
wurinsa, ya zaɓi guda goma sha biyu daga cikinsu, waɗanda ya kira su, Manzanni.

14 Siman (wanda ya kira Bitrus), ɗan'uwansa Andarawus,
Yaƙub,
Yohanna,
Filibus,
Bartolomeyu,
15 Mattiyu,
Toma,
Yaƙub ɗan Alfayus,
Siman wanda ake kira Zilot,
16 Yahuda ɗan Yaƙub,
da kuma Yahuda Iskariyot, wanda ya bashe Yesu.

*Albarku da la'anu*
*(Mattiyu 4.23-25)*
17 Sai ya sauko tare da su, ya tsaya a wani fili. A can, akwai taro mai yawa na
almajiransa, da kuma mutane masu yawan gaske daga ko'ina a Yahudiya, Urushalima
da kuma Taya da Sidon da suke bakin teku, 18 waɗanda suka zo domin su ji shi, a
kuma warkar da cututtukansu. Waɗanda suke fama da mugayen ruhohi kuwa aka
warkar da su. 19 Kuma dukan mutane suka yi ƙoƙari su taɓa shi, domin iko yana
fitowa daga gare shi, ya kuwa warkar da su duka.
*(Mattiyu 5.1-12)*
20 Da ya dubi almajiransa, sai ya ce,
"Masu albarka ne ku da kuke matalauta,

gama mulkin Allah naku ne.
21 Masu albarka ne ku da kuke jin yunwa yanzu,
gama za ku ƙoshi.
Masu albarka ne ku da kuke kuka yanzu,
gama za ku yi dariya.
22 Masu albarka ne sa'ad da mutane suka ƙi ku,
suka ware ku, suka zage ku,
suna ce da ku mugaye,
saboda Ɗan Mutum.
23 "Ku yi farin ciki a wannan rana, ku kuma yi tsalle don murna, saboda ladarku
yana da yawa a sama. Gama haka kakanninsu suka yi wa annabawa.
24 "Amma kaitonku da kuke da arziki,
gama kun riga kun sami ta'aziyyarku.
25 Kaitonku da kuke ƙosassu yanzu,
gama za ku zauna da yunwa.
Kaitonku da kuke dariya yanzu,
gama za ku yi makoki da kuka.
26 Kaitonku sa'ad da dukan mutane suna magana mai kyau a kanku,
gama haka kakanninsu suka yi da annabawan ƙarya.

### *Kaunar abokan gāba*
### *(Mattiyu 5.38-48; 7.12)*

27 "Amma ina faɗa muku, ku da kuke ji na, ku ƙaunaci abokan gābanku, ku yi
wa masu ƙinku alheri. 28 Ku albarkaci waɗanda suke la'anta ku, ku kuma yi wa
waɗanda suke wulaƙanta ku addu'a. 29 In wani ya mare ka a wannan kumatu, juya
masa ɗayan ma, in wani ya ƙwace maka babban riga, kada ma ka hana masa 'yar
cikin ma. 30 Duk wanda ya roƙe ka abu, ka ba shi. In kuma wani ya yi maka ƙwace,
kada ka nema yǎ mayar maka. 31 Ka yi wa waɗansu abin da kai kake so su yi maka.
32 "In kana ƙaunar masu ƙaunarka ne kawai, ina ribar wannan? Ko masu zunubi
ma suna ƙaunar waɗanda suke ƙaunarsu. 33 In kuma kana yin alheri ga masu yi
maka ne kaɗai, ina ribar wannan? Ko masu zunubi ma suna yin haka. 34 In kana ba
da bashi ga mutanen da za su iya biyan ka ne kawai, ina ribar wannan? Ko masu
zunubi ma, suna ba da bashi ga masu zunubi, da fata za a biya su tsab. 35 Amma, ku
ƙaunaci abokan gābanku, ku kuma yi musu alheri, ku ba su bashi, ba da sa zuciya
sai an biya ku ba. Ta yin haka ne kawai, za ku sami lada mai yawa, ku kuma zama
'ya'yan Mafi Ɗaukaka, gama shi mai alheri ne ga marasa godiya da mugaye. 36 Ku
zama masu jinƙai, kamar yadda Ubanku mai jinƙai ne.

### *Ba wa waɗansu laifi*
### *(Mattiyu 7.1-5)*

37 "Kada ku ɗora wa wani, ku ma ba za a ɗora muku ba. Kada ku yanke wa wani
hukunci, ku ma ba za a yanke muku ba. Ku gafarta, ku ma za a gafarta muku. 38 Ku
bayar, ku ma sai a ba ku mudu a cike, a danƙare, har yǎ yi tozo, yana zuba, za a juye
muku a hannun riga. Mudun da kuka auna da shi, da shi za a auna muku."
39 Ya kuma faɗa musu wannan misali cewa, "Makaho yana iya jagoran makaho ne?
Ba sai dukansu biyu su fāɗa a rami ba? 40 Ɗalibi bai fi malaminsa ba, sai dai kowane
ɗalibi wanda ya sami cikakkiyar koyarwa, zai zama kamar malaminsa.
41 "Don me kake duban ɗan tsinke da yake idon ɗan'uwanka, amma ba ka kula
da gungumen da yake a naka ido ba? 42 Yaya za ka ce wa ɗan'uwanka, 'Ɗan'uwa,
bari in cire maka ɗan tsinke da yake idonka,' alhali kuwa, kai kanka ka kāsa ganin

gungumen da yake a naka ido? Kai munafuki! Ka fara cire gungumen daga idonka, sa'an nan za ka iya gani sosai, ka kuma cire ɗan tsinken da yake a idon ɗan'uwanka."

### *Itace da 'ya'yansa*
### *(Mattiyu 7.17-20; 12.34,35)*

43 "Ba itace mai kyau da yake ba da munanan 'ya'ya. Mummunan itace kuma
ba ya ba da 'ya'ya masu kyau. 44 Kowane itace da irin 'ya'yansa ne ake saninsa.
Mutane ba sa tsinke 'ya'yan ɓaure daga ƙaya, ko kuwa 'ya'yan inabi daga sarƙaƙƙiya.
45 Mutumin nagari yakan nuna abubuwa nagari daga cikin nagarta da yake a ɓoye
a zuciyarsa, mugun mutum kuwa yakan nuna mugayen abubuwa daga muguntar da
take a ɓoye a zuciyarsa. Gama baki yakan faɗa abin da ya cika zuciya ne."

### *Mai gini mai hikima da mai gini marar hikima*
### *(Mattiyu 7.24-27)*

46 "Don me kuke ce da ni, 'Ubangiji, Ubangiji,' amma ba kwa yin abin da na faɗa?
47 Zan nuna muku kwatancin mutumin da yakan zo wurina, yă ji kalmomina, yă
kuma aikata. 48 Yana kama da mutumin da ya gina gida, wanda ya haƙa ƙasa da
zurfi, sa'an nan ya kafa tushen ginin a kan dutse. Da ambaliyar ruwa ta taso, ƙarfin
ruwa kuwa ya buga gidan, wannan bai jijjiga shi ba, domin an yi masa tushen gini
na ainihi. 49 Amma wanda yakan ji kalmomina, ba ya kuma aikata su, yana kama da
mutumin da ya gina gida a ƙasa, ba tare da ya kafa tushen gini ba. A sa'ad da ƙarfin
ruwa ya buga gidan, sai gidan yă rushe, mummunar rushewa kuwa."

## 7

### *Bangaskiyar jarumin Roma*
### *(Mattiyu 8.5-13; Yohanna 4.43-54)*

1 Bayan Yesu ya gama gaya wa mutanen dukan waɗannan abubuwa, sai ya shiga
Kafarnahum. 2 A can, akwai wani bawan wani jarumin yana ciwo, yana kuma a
bakin mutuwa. Maigidansa kuwa yana sonsa sosai. 3 Jarumin sojan ya ji labarin Yesu,
sai ya aiki waɗansu dattawan Yahudawa wajensa, yana roƙonsa yă zo yă warkar da
bawansa. 4 Da suka isa wurin Yesu, sai suka roƙe shi sosai, suka ce, "Wannan mutum,
ai, ya dace a yi masa haka, 5 gama yana ƙaunar al'ummarmu ta Yahudawa, har ya
gina majami'armu." 6 Sai Yesu ya tafi tare da su.

Da ya yi kusa da gidan, sai jarumin nan, ya aiki abokai su ce masa, "Ubangiji, kada
ka dami kanka, gama ban isa ka shiga gidana ba. 7 Shi ya sa ban ma ga na isa in zo
wurinka ba. Amma ka yi magana kawai, bawana zai warke. 8 Gama ni kaina, mutum
ne a ƙarƙashin iko, akwai kuma sojoji a ƙarƙashin ikona. Nakan ce wa wannan, 'Je
ka,' sai yă tafi, ga wani kuma in ce, 'Zo nan,' sai yă zo. Nakan kuma ce wa bawana,
'Yi abu kaza,' sai yă yi."

9 Da Yesu ya ji haka, sai ya yi mamaki sosai. Ya juya ya wa taron da yake bin sa,
"Ina faɗa muku, ban taɓa samun irin bangaskiya mai girma haka ko cikin Isra'ila
ba." 10 Sai mutanen da aka aika, suka koma gida, suka tarar bawan ya warke.

### *Yesu ya tā da ɗan gwauruwa*

11 Ba a daɗe ba, sai Yesu ya tafi wani garin da ake kira Nayin. Almajiransa da taro
mai yawa suka tafi tare da shi. 12 Da ya yi kusa da ƙofar garin, sai ga wata gawa
ana fitowa da ita. Shi ne ɗa kaɗai ga mahaifiyarsa, ita kuma gwauruwa ce. Taro mai
yawa daga garin yana tare da ita. 13 Da Ubangiji ya gan ta, sai ya ji tausayinta ya ce,
"Kada ki yi kuka."

14 Yesu ya je ya taɓa akwatin gawar, sai masu ɗaukarsa suka tsaya cik. Sai ya ce,
"Saurayi, na ce maka, tashi!" 15 Sai mamacin ya tashi zaune, ya fara magana. Yesu
kuma ya ba da shi ga mahaifiyarsa.
16 Sai tsoro ya kama su duka, suka yabi Allah, suna cewa, "Babban annabi ya
bayyana a cikinmu. Allah ya zo domin yă taimaki mutanensa." 17 Wannan labarin
game da Yesu, ya bazu ko'ina a Yahudiya da kewayenta.

### *Yesu da Yohanna Mai Baftisma (Mattiyu 11.1-19)*

18 Almajiran Yohanna suka gaya masa dukan waɗannan abubuwa. Sai ya kira biyu
daga cikinsu, 19 ya aike su wurin Ubangiji, su tambaya su ce, "Kai ne wanda zai zo,
ko kuma mu saurari wani dabam?"
20 Da mutanen suka iso wurin Yesu, sai suka ce, "Yohanna Mai Baftisma ne ya aike
mu wurinka, mu yi tambaya, 'Ko kai ne wanda zai zo, ko kuma mu saurari wani
dabam?' "
21 A daidai lokacin nan, Yesu ya warkar da mutane da yawa masu ciwo, masu
cututtuka, da kuma masu mugayen ruhohi. Ya kuma ba makafi da yawa ganin gari.
22 Sai ya amsa wa almajiran Yohanna ya ce, "Ku koma ku faɗa wa Yohanna abin
da kuka ji, da abin da kuka gani. Makafi suna ganin gari, guragu suna tafiya, ana
warkar da waɗanda suke da kuturta, kurame suna ji, ana tā da matattu, ana kuma
yi wa matalauta wa'azin bishara. 23 Mai albarka ne mutumin da bai yi shakkar
bangaskiyar da yake da ita a kaina ba."
24 Bayan almajiran Yohanna suka tafi, sai Yesu ya fara yi wa taron magana game da
Yohanna ya ce, "Me kuka je kallo a hamada? Ciyawar da iska take kaɗawa ne? 25 In
ba haka ba, to, me kuka je kallo? Mutum mai sanye da tufafi masu kyau ne? A'a,
masu sa kayan tsada da suke cikin annashuwa, ai, a fada suke. 26 Amma me kuka je
kallo? Annabi? I, ina kuma faɗa muku, ya ma fi annabi. 27 Wannan shi ne wanda
aka rubuta game da shi cewa,
" 'Zan aiko da ɗan saƙona yă sha gabanka,
wanda zai shirya hanya, a gabanka.'*
28 Ina faɗa muku, a cikin duk waɗanda mata suka haifa, ba wanda ya fi Yohanna
girma. Duk da haka wanda ya fi ƙasƙanta a Mulkin Allah ya fi shi."
29 (Dukan mutane, har da masu karɓar haraji, da suka ji kalmomin Yesu, sai
suka yarda cewa hanyar Allah gaskiya ce, domin Yohanna ne ya yi musu baftisma.
30 Amma Farisiyawa da masanan dokoki, suka ƙi nufin Allah game da su, domin
Yohanna bai yi musu baftisma ba.)
31 Yesu ya ci gaba da cewa, "To, da me zan kwatanta mutanen zamanin nan? Kamar
me suke? 32 Suna kama da yaran da suke zama a bakin kasuwa, suna kiran juna, suna
cewa,
" 'Mun busa muku sarewa,
amma ba ku yi rawa ba,
Mun kuma yi muku waƙar makoki,
ba ku kuma yi kuka ba.'
33 Gama Yohanna Mai Baftisma ya zo, ba ya cin burodi, ba ya shan ruwan inabi, sai
kuka ce, 'Ai, yana da aljani.' 34 Ɗan Mutum ya zo yana ci, yana sha, sai kuka ce,
'Ga mai yawan ci, mashayi, da kuma abokin masu karɓar haraji da masu zunubi.'
35 Amma akan tabbatar da hikima ta gaskiya bisa ga dukan 'ya'yanta."

### *Mace mai zunubi ta shafe wa Yesu turare*

* **7:27** Mal 3.1

36 To, ana nan, sai ɗaya daga cikin Farisiyawa ya gayyaci Yesu cin abincin yamma
a gidansa, ya kuwa tafi gidan Bafarisiyen, ya zauna a tebur. 37 Da wata mace wadda
ta yi rayuwar zunubi a wannan gari ta ji Yesu yana cin abinci a gidan Bafarisiyen, sai
ta kawo ɗan tulun turaren alabasta, 38 ta kuma tsaya daga bayansa, wajen ƙafafunsa
tana kuka, sai hawayenta sun fara zuba a ƙafafunsa. Sai ta goge su da gashin kanta,
ta sumbace su, sa'an nan ta shafa musu turare.

39 Da Bafarisiyen da ya gayyace shi, ya ga wannan, sai ya ce a ransa, "Da mutumin
nan annabi ne, da ya san ko wace ce take taɓansa, da kuma irin macen da take, cewa
mai zunubi ce."

40 Sai Yesu ya ce masa, "Siman, ina da abin da zan faɗa maka."

Shi kuwa ya ce, "Malam sai ka faɗa."

41 Yesu ya ce, "An yi waɗansu mutum biyu da suke riƙe bashin mai ba da rance.
Ana bin guda dinari ɗari biyar, ɗayan kuma hamsin. 42 Dukan biyun suka gagara
biyansa, sai ya yafe musu. To, a ganinka, wa zai fi ƙaunar mutumin nan?"

43 Siman ya amsa ya ce, "A ganina, wanda aka yafe wa mai yawa ne."

Sai Yesu ya ce, "Ka faɗa daidai."

44 Sai ya juya wajen macen, ya ce wa Siman, "Ka ga macen nan? Na shigo gidanka,
ba ka ba ni ruwa don ƙafafuna ba, amma ta wanke ƙafafuna da hawayenta, ta kuma
goge su da gashin kanta. 45 Ba ka yi mini sumba ba, amma tun shigowata a nan,
macen nan ba tă daina sumbar ƙafafuna ba. 46 Ba ka shafa mai a kaina ba, amma ta
zubo turare a ƙafafuna.

47 "Saboda haka ina gaya maka, zunubanta masu yawa, an gafarta mata, gama
ƙaunarta mai yawa ce. Amma wanda aka gafarta wa kaɗan kuwa, yakan nuna
ƙauna kaɗan."

48 Sai Yesu ya ce mata, "An gafarta miki zunubanki."

49 Sauran baƙin suka fara ce wa juna, "Wane ne wannan, wanda har yake gafarta
zunubai?"

50 Yesu ya ce wa macen, "Bangaskiyarki ta cece ki, ki sauka lafiya."

# 8

*Misalin mai shuka*

1 Bayan wannan sai Yesu ya zazzaga gari da ƙauye, yana wa'azin bisharar mulkin
Allah. Sha Biyun nan kuwa suna tare da shi, 2 da kuma waɗansu mata waɗanda
aka warkar da su daga cututtukansu, da kuma mugayen ruhohi. Cikinsu akwai
Maryamu (wadda ake kira Magdalin) wadda aljanu bakwai suka fito daga cikinta.
3 Da Yowanna matar Kuza, manajan iyalin Hiridus; da Suzana; da waɗansu mata da
yawa. Waɗannan mata suna taimaka musu cikin hidima, daga cikin abin da suke da
shi na zaman gari.

*(Mattiyu 13.1-9; Markus 4.1-9)*

4 Yayinda taron mai girma na taruwa, mutane kuma daga garuruwa dabam-dabam
suna zuwa wurin Yesu, sai ya ba da wannan misali ya ce, 5 "Wani manomi ya fita
domin ya shuka irinsa. Da yana watsa irin, sai waɗansu suka fāɗi a kan hanya, aka
tattaka su, tsuntsayen sararin sama kuma suka cinye su. 6 Waɗansu suka fāɗi a kan
dutse, da suka tsira sai suka yanƙwane don babu ruwa a wurin. 7 Waɗansu kuma
suka fāɗi a cikin ƙaya. Da suka yi girma tare, sai ƙayan suka shaƙe su. 8 Waɗansu
kuma har yanzu, suka fāɗi a ƙasa mai kyau, suka yi girma, suka ba da amfani riɓi
ɗari-ɗari, fiye da abin da aka shuka."

Da faɗin haka sai ya ce, "Duk mai kunnen ji, yă ji."

*(Mattiyu 13.10-17; Markus 4.10-12)*

[9] Almajiransa suka tambaye shi ma’anar wannan misali. [10] Sai ya ce, “Ku ne aka
ba sanin asirin mulkin Allah, amma ga sauran mutane kam, ina magana da misalai,
saboda,
“ ‘ko da yake suna kallo, ba za su gani ba,
ko da yake suna ji, ba za su gane ba.’

*(Mattiyu 13.18-23; Markus 4.13-20)*

[11] “Ga ma’anar misalin, irin, shi ne maganar Allah. [12] Waɗanda suka fāɗi a kan
hanya su ne mutanen da suka ji, amma Iblis, yakan zo ya ɗauke maganar daga
zuciyarsu, don kada su gaskata, su sami ceto. [13] Na kan dutse kuwa, su ne da jin
maganar, sukan karɓa da murna, amma ba su da saiwa. Sukan gaskata na ɗan
lokaci, amma lokacin gwaji, sai su ja da baya. [14] Irin da suka fāɗi a cikin ƙaya kuwa,
su ne mutanen da suka ji, amma a kwana a tashi, tunanin kayan duniya, da neman
arziki, da son jin daɗi, sukan hana su ba da ’ya’ya. [15] Amma irin da suka fāɗi a ƙasa
mai kyau kuwa, su ne mutane masu kyakkyawar zuciya, mai kyau, da suka ji, suka
riƙe, suka kuma jimre har suka ba da ’ya’ya.”

*Fitila a kan wurin ajiye fitila*
*(Markus 4.21-25)*

[16] “Ba mai ƙuna fitila sa’an nan ya ɓoye ta a cikin tulu, ko kuma ya sa ta a ƙarƙashin
gado ba. A maimakon haka, yakan sa ta a kan wurin ajiye fitila, saboda mutane masu
shigowa su ga haske. [17] Ba abin da yake ɓoye da ba za a fallasa ba. Kuma ba abin da
yake rufe, da ba za a sani ba, ko a fitar da shi a fili ba. [18] Saboda haka, ku yi tunani
da kyau yadda kuke saurara. Duk wanda yake da shi, za a ƙara masa, duk wanda ba
shi da shi kuma, abin da yake tsammani yana da shi ma, za a karɓe daga gare shi.”

*Mahaifiyar Yesu da ’yan’uwansa*
*(Mattiyu 12.46-50; Markus 3.31-35)*

[19] Sai uwar Yesu da ’yan’uwansa suka zo, domin su gan shi, amma ba su iya
zuwa kusa da shi ba, saboda taron. [20] Sai wani ya faɗa masa cewa, “Ga uwarka
da ’yan’uwanka suna tsaye a waje suna so su gan ka.”
[21] Ya amsa ya ce, “Mahaifiyata da ’yan’uwana, su ne waɗanda suke jin maganar
Allah, suna kuma aikata ta.”

*Yesu ya kwantar da ruwa da iska*
*(Mattiyu 8.23-27; Markus 4.35-41)*

[22] Wata rana Yesu ya ce wa almajiransa, “Mu haye zuwa wancan gefen tafkin.” Sai
suka shiga jirgin ruwa suka fara tafiya. [23] Da suna cikin tafiya, sai barci ya kwashe
shi. Sai wata babban iska ta taso kan tafkin, har ruwa ya fara shiga cikin jirgin. Suka
shiga babban hatsari.
[24] Almajiran suka je suka tashe shi daga barci, suka ce, “Ubangiji, Ubangiji, za mu
nutse!”
Ya tashi ya kwaɓe iskar da kuma haukar ruwan. Sai ruwan da iskar suka natsu.
Kome ya yi tsit. [25] Sai ya tambayi almajiransa, “Ina bangaskiyarku?”
A cikin tsoro da mamaki, suka ce wa junansu, “Wane ne wannan? Yana ba da
umarni ga iska da ruwa ma, kuma suna biyayya da shi?”

*Warkar da mai aljanu*
*(Mattiyu 8.28-34; Markus 5.1-20)*

[26] Suka shiga jirgin ruwa zuwa yankin Gerasenawa da yake a hayin tafkin, daga
wajen Galili. [27] Da Yesu ya sauka daga jirgin, sai ga wani mutum mai aljanu daga
garin. Mutumin ya daɗe bai sa tufafi ba, kuma ba ya zama a gida. Yana zama a cikin
kaburbura. [28] Da ya ga Yesu, sai mutumin ya ɗaga murya da ƙarfi, ya fāɗi a gabansa,

yana ihu cewa, “Ina ruwanka da ni, Yesu, Ɗan Allah Mafi Ɗaukaka? Ina roƙonka,
kada ka ba ni wahala!” 29 Gama Yesu ya riga ya umarci mugun ruhun ya fita daga
mutumin. Sau da yawa mugun ruhun ya sha kamunsa. Ko da yake akan daure shi
hannu da ƙafa, da sarƙa, a kuma yi gadinsa, amma yakan tsinke sarƙoƙinsa, aljanun
kuma su kore shi zuwa wuraren kaɗaici, inda ba kowa.
30 Yesu ya tambaye shi, “Mene ne sunanka?”
Sai ya amsa, “Tuli,”[*] gama aljanu masu ɗumbun yawa ne suna cikinsa. 31 Suka yi
ta roƙonsa kada yǎ umarce su su shiga ramin Abis.
32 A wurin kuwa, akwai babban garken aladu da suke kiwo a gefen tudu. Aljanun
suka roƙi Yesu ya bar su, su shiga cikin aladun, ya kuwa yardar musu. 33 Da aljanun
suka fita daga cikin mutumin, sai suka shiga cikin aladun. Garken kuma ya gangara
daga kan tudun zuwa cikin tafkin, kuma suka nutse.
34 Da masu kiwon aladun suka ga abin da ya faru, sai suka ruga da gudu zuwa
garin da kewaye suka kai labari. 35 Mutanen kuma suka fito don su ga abin da ya
faru. Da suka iso wurin Yesu, sai suka tarar da mutumin da aljanun suka fita daga
cikinsa, yana zaune kusa da Yesu sanye da tufafi, kuma cikin hankalinsa, sai tsoro ya
kama su. 36 Waɗanda suka ga abin da faru, suka gaya wa mutanen yadda aka warkar
da mai aljanun. 37 Sai dukan mutanen yankin Gerasenawa suka roƙi Yesu ya bar su,
don sun tsorata sosai. Sai Yesu ya shiga jirgin ruwa ya tafi.
38 Mutumin da aka fitar da aljanun daga cikinsa, ya roƙi Yesu don yǎ tafi tare da
shi, amma Yesu ya sallame shi ya ce, 39 “Koma gida, ka shaida babban alherin da
Allah ya yi maka.” Sai mutumin ya tafi yana faɗin abin da Yesu ya yi masa a duk
garin.

### *Yarinya da ta mutu da mace marar lafiya*
### *(Mattiyu 9.18-26; Markus 5.21-43)*

40 Da Yesu ya koma, taron suka marabce shi, don dā ma duk suna jiransa. 41 Sai
wani mutum mai suna Yayirus, wani mai mulkin majami’a, ya zo ya fāɗi a gaban
Yesu, yana roƙonsa ya zo gidansa, 42 domin diyarsa ɗaya tak, wadda ta kai shekara
goma sha biyu, tana bakin mutuwa. Da Yesu yake kan hanyarsa, taron mutane masu
yawa suka yi ta matsa shi a kowane gefe. 43 A wurin kuwa, akwai wata mace wadda
tana da ciwon zubar da jini, har na shekara goma sha biyu, amma babu wanda ya
iya warkar da ita. 44 Sai ta zo ta bayansa, ta taɓa bakin rigarsa. Nan da nan, zubar
da jininta ya tsaya.
45 Yesu ya yi tambaya, “Wa ya taɓa ni?”
Bayan kowa ya yi musu, sai Bitrus ya ce, “Ubangiji, ai, mutane da yawa suna
matsinka ta kowane gefe.”
46 Amma Yesu ya ce, “Wani ya taɓa ni, na san cewa iko ya fita daga wurina.”
47 Sai macen, da ta ga ba halin ɓoyewa, sai ta fita, jikinta na rawa, ta fāɗi a gabansa.
A gaban dukan mutanen, ta faɗi dalilin da ya sa ta taɓa shi, da yadda ta warke nan
take. 48 Sai Yesu ya ce mata, “Diyata, bangaskiyarki ta warkar da ke. Ki sauka lafiya.”
49 Yayinda Yesu na cikin magana har yanzu, sai ga wani daga gidan Yayirus, mai
mulkin majami’ar ya ce, “Kada ka ƙara damun malam, diyarka ta rasu.”
50 Da Yesu ya ji wannan, sai ya ce wa Yayirus, “Kada ka ji tsoro, ka gaskata, za a
kuma warkar da ita.”
51 Da ya iso gidan Yayirus, sai ya hana kowa yǎ bi shi cikin ɗakin, sai dai Bitrus,
da Yohanna, da Yaƙub, da kuma mahaifin da mahaifiyar. 52 Ana cikin haka, dukan
mutanen kuma sai kuka da makoki suke ta yi, domin yarinyar. Sai Yesu ya ce, “Ka
daina yin kuka, ba tǎ mutu ba, tana barci ne.”

---
[*] **8:30** Lejiyon yana nufin Tuli.

53 Sai suka yi masa dariya, da yake sun san cewa, ta mutu. 54 Amma Yesu ya kama
ta a hannu ya ce, "Diyata, tashi." 55 Ruhunta ya dawo, kuma ta tashi, nan take. Yesu
ya ce musu, su ba ta wani abu tă ci. 56 Iyayenta suka yi mamaki, amma ya ba su
umarni kada su faɗa wa kowa abin da ya faru.

# 9

*Yesu ya aiki sha biyun*
*(Mattiyu 10.5-15; Markus 6.7-13)*

1 Bayan da Yesu ya tara Sha Biyun wuri ɗaya, sai ya ba su iko da izini na fitar da
dukan aljanu, da na warkar da cututtuka. 2 Ya kuma aike su, su yi wa'azin mulkin
Allah, su kuma warkar da marasa lafiya. 3 Ya ce musu, "Kada ku ɗauki kome don
tafiyar, wato, ba sanda, ba jaka, ba burodi, ba kuɗi, ba riga na biyu. 4 Duk gidan da
kuka sauka, ku zauna nan sai kun bar garin. 5 In mutane ba su karɓe ku ba, sa'ad da
kun bar garinsu, ku karkaɗe ƙurar ƙafafunku don shaida a kansu." 6 Sai suka tashi
suka shiga ƙauye zuwa ƙauye suna wa'azin bishara, suna warkar da marasa lafiya
a ko'ina.

*(Mattiyu 14.1-12; Markus 6.14-29)*

7 Yanzu fa, Hiridus mai sarauta ya ji labarin dukan abubuwan da suke faruwa. Sai
ya rikice, don waɗansu mutane suna cewa, Yohanna Mai Baftisma ne ya tashi daga
matattu, 8 waɗansu kuma suna cewa, annabi Iliya ne ya sāke bayyana. Waɗansu
kuma har wa yau, suna cewa, ɗaya daga cikin annabawa na dā ne, ya tashi. 9 Amma
Hiridus ya ce, "Yohanna dai na yanke kansa, amma wanne mutum ne nake jin labarin
abubuwan nan a kansa?" Sai ya yi ƙoƙari ya ga Yesu.

*Yesu ya ciyar da dubu biyar*
*(Mattiyu 14.13-21; Markus 6.30-44; Yohanna 6.1-14)*

10 Da manzannin suka dawo, sai suka faɗa wa Yesu abin da suka yi. Sai ya ɗauke
su, suka keɓe kansu su kaɗai, zuwa wani gari da ake kira Betsaida. 11 Amma taron
mutane suka ji labari, sai suka bi shi. Ya marabce su, kuma ya yi musu magana a
kan mulkin Allah, ya kuma warkar da masu bukatar warkarwa.

12 Da rana ta kusa fāɗuwa, sai Sha Biyun suka zo wurinsa, suka ce, "Ka sallami
taron domin su shiga ƙauyuka na kewaye, su nemi abin da za su ci, da wurin kwana,
don inda muke, ba kowa."

13 Yesu ya ce, "Ku, ku ba su wani abu su ci."

Sai suka ce masa, "Muna da burodi biyar da kifi biyu kaɗai. Sai dai, in mun je mu
sayi abinci domin dukan wannan taron." 14 Maza kaɗai sun kai kusan dubu biyar.

Amma ya ce wa almajiransa, "Ku sa su su zauna a ƙungiya hamsin-hamsin."
15 Haka almajiran suka yi, kowa kuwa ya zauna. 16 Sai Yesu ya ɗauki burodin biyar
da kifin biyun, ya ɗaga kansa sama, ya yi godiya, ya kuma kakkarya su. Ya ba
wa almajiransa, domin su rarraba wa mutanen. 17 Duka kuwa suka ci suka ƙoshi.
Almajiran suka kwashe ragowar gutsattsarin cike da kwanduna goma sha biyu.

*Shaidar Bitrus a kan Yesu*
*(Mattiyu 16.13-19; Markus 8.27-29)*

18 Wata rana sa'ad da Yesu yana addu'a a ɓoye, almajiransa kuma suna tare da shi,
sai ya tambaye, su ya ce, "Wa, taron mutane ke ce da ni?"

19 Suka amsa, suka ce, "Waɗansu suna cewa, Yohanna Mai Baftisma, waɗansu kuma
annabi Iliya, har wa yau waɗansu suna cewa, kai ɗaya daga cikin annabawan da ne,
da ya tashi da rai."

20 "Amma ku fa, wa, kuke ce da ni?"

Bitrus ya amsa ya ce, “Kiristi na Allah.”
*(Mattiyu 16.20-28; Markus 8.30–9.1)*
21 Yesu ya gargaɗe su da ƙarfi, kada su gaya wa kowa wannan magana. 22 Ya sāke
cewa, “Dole ne Ɗan mutum ya sha wahaloli da yawa, dattawa, da manyan firistoci,
da malaman dokoki kuma su ƙi shi, kuma dole a kashe shi, a rana ta uku kuma a tā
da shi da rai.”
23 Sai ya ce wa dukansu, “In wani zai bi ni, dole yă mūsanta kansa, ya ɗauki
gicciyensa kowace rana, ya bi ni. 24 Gama duk mai son ceton ransa zai rasa shi,
amma duk wanda ya rasa ransa saboda ni zai same shi. 25 Ina amfani, in mutum ya
ribato duniya duka, amma ya rasa ransa, ko kuma ya yi hasarar ransa. 26 Duk wanda
yake jin kunyana da na kalmomina, Ɗan Mutum ma zai ji kunyarsa sa'ad da zai zo
a cikin ɗaukakarsa, da ɗaukakar Uban, da kuma ta tsarkaka mala'ikun.
27 “Gaskiya nake gaya muku, waɗansu da suke tsattsaye a nan ba za su ga mutuwa
ba, sai sun ga mulkin Allah.”

### *Sāke kamanni*
*(Mattiyu 17.1-8; Markus 9.2-8)*
28 Bayan kamar kwana takwas da yin wannan magana, sai Yesu ya ɗauki Bitrus,
da Yohanna, da kuma Yaƙub, suka hau kan dutse tare don yin addu'a. 29 Yana cikin
addu'a, sai kamannin fuskarsa ta sāke, tufafinsa kuma suka zama da haske kamar
hasken walƙiya. 30 Sai ga mutum biyu, Musa da Iliya, suka bayyana cikin kyakkyawar
daraja, suna magana da Yesu. 31 Suka yi zance a kan tashinsa, wanda shi ya kusan
ya kawo ga cikarsa a Urushalima. 32 Barci kuwa ya kama Bitrus da abokan tafiyarsa
sosai. Da idanunsu suka warware, sai suka ga ɗaukakarsa da kuma mutum biyun
tsaye tare da shi. 33 Da mutanen na barin Yesu, sai Bitrus ya ce masa, “Ubangiji, ya
yi kyau da muke nan. Bari mu kafa bukkoki guda uku, wato, ɗaya dominka, ɗaya
domin Musa, ɗaya kuma domin Iliya.” (Bai ma san abin da yake faɗi ba.)
34 Yayinda yake cikin magana, sai wani girgije ya bayyana ya rufe su, sai suka ji
tsoro, yayinda suke shiga cikin girgijen. 35 Wata murya ta fito daga cikin girgijen,
tana cewa, “Wannan Ɗana ne, zaɓaɓɓena, ku saurare shi.” 36 Da muryar ta gama
magana, sai suka tarar Yesu shi kaɗai ne. Almajiran kuwa suka riƙe wannan al'amari
a zukatansu. A lokacin nan, ba su gaya wa kowa abin da suka gani ba.

### *Warkar da yaro mai mugun ruhu*
*(Mattiyu 17.14-18; Markus 9.14-27)*
37 Kashegari, sa'ad da Yesu tare da almajiran nan uku suka sauka daga kan dutsen,
sai taro mai yawa ya haɗu da shi. 38 Sai wani mutum daga cikin taron ya yi kira da
ƙarfi ya ce, “Malam, ina roƙonka, ka dubi ɗan nan nawa, gama shi ne kaɗai nake da
shi. 39 Wani ruhu yakan kama shi, sai ya yi ihu farar ɗaya. Yakan sa shi farfaɗiya,
har bakinsa ya yi kumfa. Da ƙyar yake barinsa, yana kuwa kan hallakar da shi. 40 Na
roƙi almajiranka su fitar da shi, amma ba su iya ba.”
41 Yesu ya amsa ya ce, “Ya karkataccen zamani marar bangaskiya, har yaushe ne
zan kasance tare da ku, ina kuma haƙuri da ku? Kawo yaronka nan.”
42 Yaron yana kan zuwa ke nan, sai aljanin ya buga shi ƙasa, cikin farfaɗiya. Amma
Yesu ya kwaɓe mugun ruhun, ya warkar da yaron, sai ya miƙa shi ga mahaifinsa.
43 Duk suka yi mamakin girman Allah.
*(Mattiyu 17.22,23; Markus 9.30-32)*
Yayinda kowa yana cikin mamakin dukan abubuwan da Yesu ya yi, sai ya ce wa
almajiransa, 44 “Ku kasa kunne da kyau ga abin da zan faɗa muku. Za a bashe Ɗan
Mutum ga hannun mutane.” 45 Amma ba su fahimci abin da yake nufi da wannan

magana ba. Ba su gane ba, don an ɓoye musu shi. Su kuwa sun ji tsoro su tambaye shi.

*Wa zai zama mafi girma?*
*(Mattiyu 18.1-5; Markus 9.33-37)*

46 Wata gardama ta tashi a tsakanin almajiran, a kan ko wane ne a cikinsu zai zama
mafi girma 47 Da yake Yesu ya san tunaninsu, sai ya ɗauki wani ƙaramin yaro, ya
sa ya tsaya kusa da shi. 48 Sai ya ce musu, "Duk wanda ya karɓi wannan ƙaramin
yaron a cikin sunana, ni ya karɓa, kuma duk wanda ya karɓe ni, ya karɓi wanda ya aiko ni ne. Gama mafi ƙanƙanta duka a cikinku, shi ne kuma mafi girma."

*(Markus 9.38-40)*

49 Sai Yohanna ya ce, "Ubangiji, mun ga wani mutum yana fitar da aljanu a cikin sunanka, muka yi ƙoƙarin hana shi, don shi ba ɗaya ba ne daga cikinmu."

50 Yesu ya ce, "Kada ku hana shi, gama duk wanda ba ya gāba da ku, naku ne."

*Hamayyar Samariyawa*

51 Da lokaci ya yi kusa da za a ɗauki Yesu zuwa sama, sai ya ɗaura niyyar tafiya
Urushalima. 52 Sai ya aiki 'yan saƙo, su yi gaba. Su kuwa, suka shiga cikin wani
ƙauyen Samariyawa, don su shirya masa abubuwa. 53 Amma mutanen ƙauyen ba su
karɓe shi ba, don yana kan hanyar zuwa Urushalima ne. 54 Da almajiransa, Yaƙub
da Yohanna suka ga haka, sai suka yi tambaya suka ce, "Ubangiji, kana so mu kira
wuta ta sauka daga sama ta hallaka su?" 55 Amma Yesu ya juya, ya kwaɓe su. 56 Sai
shi da almajiransa suka tafi wani ƙauye.

*Wahalar bin Yesu*
*(Mattiyu 8.19-22)*

57 Suna kan tafiya a hanya, sai wani mutum ya ce masa, "Zan bi ka, duk inda za ka."

58 Yesu ya ce, "Yanyawa suna da ramummuka, tsuntsayen sararin sama suna da sheƙuna, amma Ɗan Mutum ba shi da wurin da zai sa kansa."

59 Ya kuma ce wa wani mutum, "Ka bi ni."

Amma mutumin ya amsa ya ce, "Ubangiji, bari in je in binne mahaifina tukuna."

60 Yesu ya ce masa, "Ka bar matattu su binne matattunsu, amma kai, ka je ka yi shelar mulkin Allah."

61 Har wa yau, wani ya ce, "Zan bi ka, Ubangiji, amma ka bar ni in je in yi bankwana da iyalina tukuna."

62 Yesu ya amsa ya ce, "Babu wani da yakan sa hannunsa a garman shanu, sa'an nan ya waiwaya baya, da ya isa ya shiga hidima a cikin mulkin Allah ba."

# 10

*Yesu ya aiki saba'in da biyu*

1 Bayan haka, Ubangiji ya naɗa waɗansu mutum saba'in da biyu, ya aike su biyu-
biyu, su riga shi yin gaba zuwa kowane gari da kowane wuri da zai shiga. 2 Ya ce
musu, "Girbi na da yawa, amma ma'aikata kaɗan ne. Saboda haka, ku roƙi Ubangijin
girbi ya aikar da ma'aikata zuwa gonarsa. 3 Ku tafi! Ina aikan ku kamar tumaki cikin
kyarketai. 4 Kada ku ɗauki jakar kuɗi, ko jaka, ko takalma. Kada ma ku gai da kowa
a kan hanya.

5 "Sa'ad da kuka shiga wani gida, ku fara da cewa, 'Salama a gare ku mutanen
gida.' 6 In akwai mutum mai salama a gidan, salamarku za tă kasance tare da shi, in
kuwa babu, salamarku za tă koma muku. 7 Ku zauna a wannan gidan, kuna ci kuna
shan duk abin da suka ba ku, gama ma'aikaci ya cancanci albashinsa. Kada ku yi
yawan sāke masauƙi, daga gida zuwa gida.

8 “Sa’ad da kuka shiga garin, kuma aka karɓe ku, ku ci ko mene ne da aka ajiye a
gabanku. 9 Ku warkar da marasa lafiya da suke wurin. Ku kuma faɗa musu cewa,
‘Mulkin Allah yana kusa da ku.’ 10 Amma sa’ad da kuka shiga garin, kuma ba a karɓe
ku ba, ku bi titi-titi ku ce, 11 ‘Ko ƙurar garinku da kuke manne a ƙafafunmu, mun
karkaɗe muku. Duk da haka, ku tabbatar da wannan, “Mulkin Allah yana kusa.” ’
12 Ina dai faɗa muku, a ranan nan, za a fi jin tausayin Sodom fiye da wannan garin.

*(Mattiyu 11.20-24)*

13 “ ‘Kaitonki, Korazin! Kaitonki, Betsaida!’ Ai, da a ce a Taya da Sidon ne aka yi
ayyukan banmamaki da aka yi a cikinku, da tuni sun tuba, suna zama cikin rigar
makoki da toka. 14 A ranar shari’a, za a fi jin tausayin Taya da Sidon fiye da ku. 15 Ke
kuma Kafarnahum, kina tsammani za ki sami ɗaukaka ne? A’a, za a hallaka ki.
16 “Wanda ya saurare ku, ni yake saurara. Wanda ya ƙi ku, ni yake ƙi. Amma
wanda ya ƙi ni kuwa, ya ƙi wanda ya aiko ni ne.”
17 Mutum saba’in da biyun nan suka dawo da murna, suka ce, “Ubangiji, har mun
sha ƙarfin aljanu ma a cikin sunanka.”
18 Sai ya amsa ya ce, “Na ga Shaiɗan ya fāɗi daga sama kamar walƙiya. 19 Na ba
ku iko da za ku tattaka macizai, da kunamai, ku kuma shawo kan dukan ikon abokin
gāba, kuma ba wani lahani da zai same ku. 20 Duk da haka, kada ku yi farin ciki da
cewa, kun sha ƙarfin ruhohi, amma ku yi farin ciki, domin an rubuta sunayenku a
sama.”

*(Mattiyu 11.20-24)*

21 A wannan lokaci, Yesu, cike da murna ta wurin Ruhu Mai Tsarki ya ce, “Na
yabe ka, ya Uba, Ubangijin sama da ƙasa, domin ka ɓoye waɗannan abubuwa ga
masu hikima, da masu ilimi, ka kuma bayyana su ga ƙananan yara. I, ya Uba, gama
wannan shi ne nufinka mai kyau.
22 “Ubana ya danƙa mini dukan kome. Ba wanda ya san Ɗan sai Uban, kuma ba
wanda ya san Uban, sai Ɗan, da kuma waɗanda Ɗan ya zaɓa ya bayyana musu shi.”
23 Sai ya juya wajen almajiransa, ya ce musu a ɓoye, “Albarka ga idanun da suka
ga abin da kuke gani. 24 Ina faɗa muku, annabawa da sarakuna da yawa sun so su
ga abin nan da kuke gani, amma ba su gani ba. Sun so su ji abin da kuke ji, amma
ba su ji ba.”

*Misalin mutumin Samariya nagari*

25 Wata rana, sai wani masanin dokoki ya miƙe tsaye don yǎ gwada Yesu. Ya
tambaya ya ce, “Malam, me zan yi don in gāji rai madawwami?”
26 Yesu ya amsa ya ce, “Me aka rubuta a cikin Doka? Yaya kake karanta ta?”
27 Sai ya amsa ya ce, “ ‘Ka ƙaunaci Ubangiji Allahnka da dukan zuciyarka, da
dukan ranka, da dukan ƙarfinka, da kuma dukan hankalinka’; kuma, ‘Ka ƙaunaci
maƙwabcinka kamar kanka.’ ”
28 Yesu ya ce, “Ka amsa daidai. Ka yi haka, kuma za ka rayu.”
29 Amma domin ya kāre kansa, sai ya tambayi Yesu ya ce, “Shin, wane ne
maƙwabcina?”
30 Yesu ya amsa ya ce, “Wani mutum ya tashi daga Urushalima za shi Yeriko, sai ya
fāɗi a hannun mafasa, wato, ’yan fashi. Suka ƙwace tufafinsa, suka yi masa dūka,
suka bar shi nan bakin rai da mutuwa. 31 Ya zamana wani firist ya bi kan wannan
hanya. Da ya ga mutumin, sai ya bi gefe ya wuce abinsa. 32 Haka ma wani daga
kabilar Lawi, mai hidima cikin haikali, da ya zo wurin, ya gan shi, sai shi ma ya bi
gefe ɗaya, ya wuce abinsa. 33 Amma wani mutumin Samariya da yake kan tafiya,
da ya kai inda mutumin yake, ya gan shi, sai ya ji tausayinsa. 34 Ya je wurinsa,
ya daddaure masa raunukansa, sa’an nan ya zuba mai, da ruwan inabi. Ya ɗauki
mutumin ya sa a kan jakinsa, ya kai shi wani masauƙi, ya yi jinyarsa. 35 Kashegari,

sai ya ɗauki dinari biyu, ya ba wa mai masauƙin ya ce, ‘Ka lura da shi, bayan na
dawo, zan biya ka duk abin da ka ƙara kashewa a kansa.’
36 “A ganinka, a cikin waɗannan mutane uku, wane ne maƙwabcin mutumin da
ya fāɗi a hannun mafasa?”
37 Masanin dokoki ya amsa ya ce, “Wanda ya nuna masa jinƙai.”
Yesu ya ce masa, “Je ka, ka yi haka nan.”

### *A gidan Marta da Maryamu*

38 Yayinda Yesu da almajiransa suna cikin tafiya, sai ya kai wani ƙauye inda wata
mace mai suna Marta ta marabce shi a gidanta. 39 Tana da ʼyarʼuwa mai suna
Maryamu, wadda ta zauna a gaban Ubangiji tana jin maganarsa. 40 Marta kuwa,
aikin hidima da ya kamata a yi, ya ɗauke mata hankali, sai ta zo wurin Yesu, ta ce,
“Ubangiji, ba ka damu da yadda ʼyarʼuwata ta bar mini aiki ni kaɗai ba? Gaya mata
ta taimake ni!”
41 Amma Ubangiji ya amsa ya ce, “Marta, Marta, hankalinki ya tashi, kuma kina
damuwa a kan abubuwa da yawa. 42 Amma abu ɗaya tak ake bukata, Maryamu ta
zaɓi abin da ya fi kyau, kuma ba za a raba ta da shi ba.”

## 11

### *Koyarwar Yesu a kan adduʼa*
*(Mattiyu 6.9-13; 7.7-11)*

1 Wata rana Yesu yana adduʼa a wani wuri. Da ya gama, sai ɗaya daga cikin
almajiransa ya ce masa, “Ubangiji, ka koya mana yin adduʼa, kamar yadda Yohanna
ya koya wa almajiransa.”
2 Sai ya ce musu, “Saʼad da kuke yin adduʼa ku ce,
“ ‘Ya Uba,
sunanka mai tsarki ne
mulkinka ya zo.
3 Ka ba mu kowace rana abincin yini.
4 Ka gafarta mana zunubanmu,
kamar yadda mu ma ke gafarta wa duk wanda ya yi mana laifi.
Kada ka bari a kai mu cikin jarraba.’ ”
5 Saʼan nan ya ce musu, “Da a ce ɗayanku yana da aboki, saʼan nan ya je wurinsa
da tsakar dare ya ce, ‘Aboki, ranta mini burodi guda uku, 6 domin wani abokina da
yake tafiya ya sauka a wurina. Ga shi, ba ni da abinci da zan ba shi.’ 7 Sai wanda
yake cikin ɗaki ya amsa ya ce, ‘Kada ka dame ni. An riga an kulle ƙofa, da ni da
yarana kuwa mun kwanta, ba zan iya tashi in ba ka kome ba.’ 8 Ina gaya muku, ko
da yake ba zai so ya tashi ya ba shi burodin don shi abokinsa ne ba, duk da haka, zai
tashi ya ba shi yawan abin da yake bukata, saboda nacewarsa.
9 “Don haka ina faɗa muku, ku roƙa, za a ba ku, ku nema za ku samu, ku
ƙwanƙwasa za a kuwa buɗe muku ƙofa. 10 Gama duk wanda ya roƙa, yana karɓa,
mai nema yana samu, wanda ya ƙwanƙwasa kuma, za a buɗe masa ƙofa.
11 “Wane mahaifi ne a cikinku, in ɗansa ya roƙe shi kifi, zai ba shi maciji a
maimakon, 12 ko kuma in ya roƙi ƙwai, ya ba shi kunama? 13 In fa haka ne, ko
da yake ku mugaye ne, kun san ba ʼyaʼyanku kyautai masu kyau, balle fa Ubanku na
sama, zai yi fiye da haka, ta wurin ba da Ruhu Mai Tsarki, ga masu roƙonsa!”

### *Yesu da Beʼelzebub*
*(Mattiyu 12.22-30; Markus 3.20-27)*

14 Saʼad da Yesu yake fitar da wani beben aljani daga wani mutum, da aljanin ya
fita, sai mutumin wanda da bebe ne, ya yi magana, taron kuwa suka yi mamaki.

15 Amma waɗansunsu suka ce, “Ai, da ikon Be’elzebub, sarkin aljanu ne, yake fitar
da aljanu.” 16 Waɗansu kuma suka gwada shi, ta wurin neman yă nuna musu wata
alama daga sama.

17 Yesu kuwa ya san tunaninsu, sai ya ce musu, “Duk mulkin da yake gāba da kansa,
zai lalace, kuma gidan da yake gaba da kansa zai rushe. 18 In Shaiɗan yana gāba da
kansa, yaya mulkinsa zai tsaya? Ina faɗin haka domin kun ce, da ikon Be’elzebub
nake fitar da aljanu. 19 In da ikon Be’elzebub nake fitar da su, to, da ikon wa masu
binku suke fitar da su? Saboda haka, za su zama alƙalanku ke nan. 20 Amma in da
ikon Allah ne ni nake fitar da aljanu, ashe, mulkin Allah ya zo muku ke nan.

21 “Sa’ad da mutum mai ƙarfi, wanda yake da makamai yana gadin gidan kansa,
an tsare lafiyar dukiyarsa ke nan. 22 Amma in wani wanda ya fi shi ƙarfi, ya faɗa
masa ya kuma sha ƙarfinsa, yakan ƙwace makaman da mutumin ke dogara da su,
ya kuma rarraba ganima.

23 “Wanda ba ya tare da ni, yana gāba da ni, wanda kuma ba ya tarawa da ni,
watsarwa yake yi.

*(Mattiyu 12.43-45)*

24 “Lokacin da mugun ruhu ya fita daga mutum, sai ya bi ta wuraren da ba mutane,
yana neman hutu, amma ya kāsa samu, sai ya ce, ‘Zan koma gidan da na bari.’
25 Sa’ad da ya koma, ya tarar da gidan a share da tsabta, kuma a shirye. 26 Sai ya
je ya ɗebo waɗansu ruhohi bakwai da suka fi shi mugunta, sai su shiga su zauna a
wurin. Karshen wannan mutum kuwa zai fi farkonsa muni.”

27 Da Yesu yake cikin faɗin waɗannan abubuwa, sai wata mace daga cikin taron ta
ɗaga murya ta ce masa, “Mai albarka ce uwar da ta haife ka, wadda ka sha mamanta.”

28 Yesu ya amsa ya ce, “A maimakon, masu albarka ne waɗanda suke jin maganar
Allah, suna kuma biyayya da ita.”

### *Alamar Yunana*

*(Mattiyu 12.38-42; Markus 8.12)*

29 Da taron mutane suka ƙaru, sai Yesu ya ce, “Wannan mugun zamani ne. Tana
neman wani abin banmamaki, amma ba ko ɗaya da za a ba ta, sai dai ta Yunana.
30 Kamar yadda Yunana ya zama alama ga mutanen Ninebe, haka ma Ɗan Mutum
zai zama ga zamanin nan. 31 A ranar shari’a, Sarauniyar Kudu za tă tashi tsaye tare
da wannan zamani, ta yanke wa wannan zamani hukunci, domin ta zo daga ƙarshen
duniya ta saurari hikimar Solomon, ga shi kuwa, shi wanda ya fi Solomon girma, na
nan. 32 A ranar shari’a, mutanen Ninebe za su tashi tsaye tare da wannan zamani,
su yanke wa wannan zamani hukunci. Gama sun tuba sa’ad da Yunana ya yi musu
wa’azi. Ga shi yanzu, shi wanda ya fi Yunana girma, na nan.

### *Fitilar jiki*

*(Mattiyu 5.15; 6.22,23)*

33 “Babu wanda yakan ƙuna fitila sa’an nan ya ɓoye ta, ko ya rufe ta da murfi
ba. A maimako, yakan ajiye ta a kan wurin ajiye fitila, don masu shiga su ga haske.
34 Idonka shi ne fitilar jikinka. Sa’ad da idanunka suna da lafiya, dukan jikinka ma
na cike da haske, amma sa’ad da idanunka suna da lahani, dukan jikinka ma na cike
da duhu. 35 Ka lura fa, kada hasken da yake cikinka ya zamana duhu ne. 36 Saboda
haka, in dukan jikinka yana cike da haske, ba inda ke da duhu, jikinka kuwa zai
kasance da haske gaba ɗaya, kamar yadda hasken fitila yake haskaka ka.”

### *La’anu a kan Farisiyawa da kuma masanan doka*

*(Mattiyu 5.15; 6.22,23)*

37 Da Yesu ya gama magana, sai wani Bafarisiye ya gayyace shi cin abinci tare da
shi. Sai kuwa ya shiga ya zauna a tebur. 38 Amma Bafarisiyen ya lura cewa, Yesu bai
wanke hannu kafin ya ci abinci ba, sai mamaki ya kama shi.

39 Sai Ubangiji ya ce masa, “Ku Farisiyawa, kukan wanke bayan kwano da kwaf,
amma a ciki kuna cike da kwaɗayi da mugunta. 40 Ku wawayen mutane! Ashe, wanda
ya yi bayan, ba shi ne kuma ya yi cikin ba? 41 Ku ba matalauta abin da yake cikin
kwano, kuma kome zai zama muku da tsabta.

42 “Kaitonku, Farisiyawa, domin kuna ba wa Allah zakka na naʼanaʼarku, da
ƙarƙashinku, da kuma sauran ganyen lambunku iri-iri, amma kun ƙyale adalci da
ƙaunar Allah. Ya kamata da kun kiyaye na ƙarshen, ban ba barin na farkon.

43 “Kaitonku, Farisiyawa, domin kun cika son wuraren zama masu daraja a
majamiʼu, da kuma yawan gaisuwa a wuraren kasuwanci.

44 “Kaitonku, domin ku kamar kaburbura ne da ba a sa musu alama ba, waɗanda
mutane suke takawa don rashin sani.”

45 Sai ɗaya daga cikin masanan dokoki ya ce wa Yesu, “Malam, in ka faɗi waɗannan
abubuwa haka, kai kuma ka zage mu ke nan.”

46 Yesu ya amsa ya ce, “Ku masanan dokoki ma, kaitonku, domin kun ɗora wa
mutane kaya masu nauyi waɗanda da ƙyar suke ɗaukawa, amma ku da kanku ba za
ku sa ko yatsa ɗaya, don ku taimake su ba.

47 “Kaitonku, domin kun gina kaburbura saboda annabawa, nan kuwa kakannin-
kakanninku ne suka kashe su. 48 Wannan ya shaida cewa kun amince da abin
da kakannin-kakanninku suka yi. Sun karkashe annabawa, ku kuma kun gina
kaburburansu. 49 Saboda haka, Allah a cikin hikimarsa ya ce, ‘Zan aika musu da
annabawa da manzanni. Za su kashe waɗansu, su kuma tsananta wa waɗansu.’
50 Saboda haka, alhakin jinin dukan annabawa da aka kashe, tun farkon duniya,
yana kan wannan zamani, 51 wato, tun daga jinin Habila, har zuwa jinin Zakariya,
wanda aka kashe tsakanin bagade da mazauni. I, ina gaya muku, alhakinsu duka
yana kan wannan zamani.

52 “Kaitonku, masanan dokoki, domin kun ɗauke mabuɗin ilimi. Ku kanku ba ku
shiga ba, kuma kun hana wa waɗanda suke shiga, su shiga.”

53 Da Yesu ya bar wurin, sai Farisiyawa da malaman dokoki suka fara gaba mai
tsanani da shi, kuma suna tsokanansa da tambayoyi. 54 Suna fakonsa, don su kama
shi a kan wata magana da zai faɗa.

# 12

### *Faɗakarwa da ƙarfafawa*

1 Ana nan saʼad da taron dubban mutane suka taru har suna tattaka juna, Yesu
fara yin magana, da farko da almajiransa ya ce, “Ku yi hankali da yistin Farisiyawa,
wato, munafunci. 2 Ba abin da yake rufe da ba za a fallasa ba, ko kuma abin da yake
ɓoye da ba za a bayyana ba. 3 Abin da kuka faɗa a cikin duhu, za a ji shi a hasken
rana. Kuma abin da kuka faɗa a kunne, a cikin ɗakunan ciki-ciki, za a yi shelarsa
daga kan rufin ɗakuna.

*(Mattiyu 10.28-31)*

4 “Ina dai gaya muku abokaina, kada ku ji tsoron masu kashe jiki, amma bayan
haka, ba sauran abin da za su iya yi. 5 Amma zan nuna muku wanda za ku ji tsoronsa.
Ku ji tsoron wanda, bayan da ya kashe jikin, yana da iko ya jefa ku cikin jahannama
ta wuta. I, ina gaya muku, ku ji tsoronsa. 6 Ba ana sayar da kanari biyar a kan kobo
biyu ba? Duk da haka, Allah bai manta da ko ɗayansu ba. 7 Tabbatacce, gashin kanku

ɗin nan ma, an ƙidaya su duka. Kada ku ji tsoro. Darajarku ta fi na kanari masu
yawa girma.

*(Mattiyu 10.32,33; 12.32; 10.19,20)*

8 “Ina gaya muku, duk wanda ya shaida ni a gaban mutane, Ɗan Mutum ma zai
shaida shi a gaban mala’ikun Allah. 9 Amma wanda ya yi mūsun sanina a gaban
mutane, shi ma za a yi mūsunsa a gaban mala’ikun Allah. 10 Kuma duk wanda ya
faɗi kalmar zagi a kan Ɗan Mutum, za a gafarta masa, amma duk wanda ya saɓa wa
Ruhu Mai Tsarki, ba za a gafarta masa ba.

11 “Sa’ad da an kai ku a gaban majami’u, da gaban masu mulki, da kuma gaban
masu iko, kada ku damu da yadda za ku kāre kanku, ko kuma abin da za ku faɗa,
12 gama Ruhu Mai Tsarki zai koya muku abin da ya dace ku faɗa a lokacin.”

*Misalin wawa mai arziki*

13 Sai wani mutum daga cikin taron ya ce masa, “Malam, ka ce wa ɗan’uwana ya
raba gādon da ni.”

14 Yesu ya amsa masa ya ce, “Kai, wa ya naɗa ni alƙali, ko mai sulhu a tsakaninku?”
15 Sai ya ce musu, “Ku lura fa! Ku tsare kanku daga dukan kowane irin kwaɗayi. Ran
mutum ba ya danganta a kan yawan dukiyarsa ba.”

16 Sai ya gaya musu wannan misali ya ce, “Gonar wani mai arziki ta ba da amfani
sosai. 17 Ya yi tunani a ransa ya ce, ‘Ba ni da inda zan ajiye amfanin gonana. Me zan
yi ke nan?’

18 “Sai ya ce, ‘Ga abin da zan yi. Zan rushe rumbunana, in gina manya, in zuba
dukan hatsina da kayana a ciki. 19 Ni kuma zan ce wa raina, “Kana da kaya da yawa
masu kyau, da aka yi ajiyarsu domin shekaru da dama masu zuwa. Yi hutunka, ka
ci, ka sha, ka yi annashuwa.” ’

20 “Amma Allah ya ce masa, ‘Kai wawa! A wannan dare za a nemi ranka. Bayan
haka, wa zai gāji abin da ka tara wa kanka?’

21 “Haka zai zama ga duk wanda ya tara wa kansa dukiya, amma ba shi da arziki
a gaban Allah.”

*Kada ku damu*

*(Mattiyu 6.25-34)*

22 Sai Yesu ya ce wa almajiransa, “Saboda haka, ina faɗa muku, kada ku damu game
da rayuwarku, abin da za ku ci, ko kuma game da jikinku, abin da za ku yafa. 23 Rai
ya fi abinci, jiki kuma ya fi tufafi. 24 Ku dubi hankaki. Ba sa shuki ko girbi, kuma
ba su da ɗakin ajiya ko rumbu ba, duk da haka, duk da haka, Allah na ciyar da su.
Darajarku ta fi na tsuntsaye sau da yawa! 25 Wane ne a cikinku ta wurin damuwarsa,
zai iya ƙara ko sa’a ɗaya ga rayuwarsa? 26 Tun da ba za ku iya yin wannan ƙanƙanin
abu ba, me ya sa kuke damuwa a kan sauran?

27 “Ku dubi yadda furanni suke girma. Ba sukan yi aiki, ko saƙa ba, duk da haka,
ina faɗa muku cewa, ko Solomon cikin kyakkyawan darajarsa duka, bai yafa kayan
ado da ya kai kamar na ko ɗaya a cikinsu ba. 28 In haka ne Allah yake yi wa ciyayin
jeji sutura, wadda yau suna nan, sa’an nan gobe kuma a jefa cikin wuta, Allah ba zai
yi muku sutura fiye da ciyayin jeji ba, ya ku masu ƙarancin bangaskiya! 29 Kada ku
sa zuciyarku a kan abin da za ku ci, ko abin da za ku sha, kada ku damu a kan su.
30 Gama duniya da ba tă san Allah ba, tana faman neman dukan waɗannan abubuwa,
Ubanku na sama kuwa, ya san kuna bukatarsu. 31 Amma ku nemi mulkinsa, za a
kuwa ƙara muku waɗannan abubuwa.

32 “Ya ƙaramin garke, kada ku ji tsoro, gama ya gamshi Ubanku ya ba ku mulkin.
33 Ku sayar da dukiyarku, ku ba wa matalauta. Ku yi wa kanku jakar kuɗin da ba za
su lalace ba. Ku yi wa kanku ajiyar dukiyar da ba za tă kare ba a sama, inda ɓarawo

ba zai yi kusa ba, asu kuma ba za su iya su lalatar ba. 34 Gama inda dukiyarku take,
nan ne zuciyarku ma take.

*Zama a faɗake*
*(Mattiyu 24.45-51)*

35 “Ku shirya ɗamara don hidima. Ku bar fitilunku suna ci, 36 kamar maza da
suke jiran maigidansu ya dawo daga bikin aure. Saboda duk lokacin da ya dawo ya
ƙwanƙwasa ƙofa, a shirye suke su buɗe masa nan da nan. 37 Zai zama da albarka
in maigida ya dawo, ya tarar da bayinsa suna zaman tsaro. Gaskiya ni faɗa muku,
zai sa kayan hidima da kansa, ya sa bayinsa su zauna kan tebur, saʼan nan ya yi
musu hidimar abinci. 38 Zai zama da albarka ga bayin da maigidansu ya iske su,
suna zaman tsaro, a duk lokacin da ya dawo, ko da ya dawo a saʼa ta biyu, ko ta uku
na tsakar dare ne. 39 Amma ku fahimci wannan. Da maigida ya san saʼar da ɓarawo
zai zo, ai, da ba zai bari a shiga, a fasa masa gida ba. 40 Ku ma, sai ku zauna da shiri,
domin Ɗan Mutum zai zo a saʼar da ba ku yi tsammani ba.”

41 Bitrus ya yi tambaya ya ce, “Ya Ubangiji, mu ne kake faɗa wa wannan misali, ko
kuwa ga kowa da kowa ne?”

42 Ubangiji ya amsa ya ce, “To, wane ne manaja mai aminci da hikima, wanda
maigida ya ba shi riƙon bayinsa, domin ya ba su abincinsu a daidai lokaci? 43 Zai
zama da albarka ga bawan nan wanda maigidan ya dawo, ya same shi yana yin haka.
44 Gaskiya nake gaya muku, maigidan zai ba shi riƙon dukan dukiyarsa. 45 Amma da a
ce bawan ya yi tunani a zuciyarsa ya ce, ‘Ai, maigidana ya yi jinkirin dawowa,’ saʼan
nan ya fara dūkan bayin, maza da mata, ya kuma shiga ci, da sha, har da buguwa.
46 Maigidan bawan nan zai dawo a ranar da wannan bawan bai yi tsammaninsa ba,
kuma a saʼar da bai sani ba. Maigidan zai yayyanka shi, ya kuma ba shi rabonsa tare
da marasa bangaskiya.

47 “Bawan da ya san nufin maigidansa, kuma bai yi shiri ba, ko kuma bai yi abin
da maigidansa yake so ba, zai sha mummunan duka. 48 Amma wanda bai sani ba, ya
kuwa yi abin da ya isa horo, za a dūke shi kaɗan. Duk wanda aka ba shi mai yawa,
mai yawan ne za a bida daga gare shi. Duk wanda kuma aka ba shi riƙon amana mai
yawa, fiye da haka kuma za a bida daga gare shi.

*Ba salama ba sai dai rabuwa*
*(Mattiyu 24.45-51)*

49 “Na zo ne domin in kawo wuta a duniya. Ina so da ta riga ta ƙunu! 50 Amma
ina da baftismar da za a yi mini, na kuwa damu sosai, sai na kammala ta! 51 Kuna
tsammani na zo domin in kawo salama a duniya ne? Aʼa! Ina gaya muku, rabuwa
ne. 52 Daga yanzu, za a iske mutum biyar a gida ɗaya sun rabu, suna gāba da juna,
uku suna gāba da biyu, biyun suna gāba da ukun. 53 Za su rarrabu. Mahaifi yana
gāba da ɗan, ɗan kuma yana gāba da mahaifin. Mahaifiya tana gāba da diyar, diyar
kuma tana gāba da mahaifiyar. Suruka tana gāba da matar ɗa, matar ɗa kuma tana
gāba da suruka.”

*Fahimtar lokuta*
*(Mattiyu 16.2,3; 5.25,26)*

54 Ya ce wa taron, “Saʼad da kuka ga hadari ya fito daga yamma, nan da nan kukan
ce, ‘Za a yi ruwan sama,’ sai a kuwa yi. 55 Saʼad da kuma iska ta taso daga kudu,
kukan ce, ‘Za a yi zafi,’ sai kuwa a yi. 56 Munafukai! Kuna san yadda za ku fassara
yanayin ƙasa da na sararin sama. Ta yaya ba ku san yadda za ku yi fassarar wannan
zamani ba?

57 “Don me ba ku iya auna wa kanku, abin da yake daidai ba? 58 Yayinda kake
kan hanyar zuwa kotu da maƙiyinka, ka yi matuƙar ƙoƙari ku shirya tun kuna kan

hanya. In ba haka ba, zai kai ka gaban alƙali, alƙali kuma ya miƙa ka ga ɗan sanda,
ɗan sanda kuma ya jefa ka a kurkuku. 59 Ina gaya maka, ba za ka fita ba, sai ka biya
kobo na ƙarshe."

# 13

### *A tuba ko a hallaka*

1 A yanzun fa, akwai waɗansu da suka kasance a lokacin can, suka ba Yesu labarin
Galiliyawa da Bilatus ya gauraye jininsu tare da jinin hadayunsu. 2 Yesu ya amsa ya
ce, "Kuna tsammani waɗannan Galiliyawan sun fi dukan sauran Galiliyawa zunubi
ne, shi ya sa suka sha irin wannan wahala? 3 Ina gaya muku, a'a! Amma in ba ku
tuba ba, ku ma duka za ku hallaka. 4 Ko kuwa kuna tsammani, sha takwas ɗin nan
da suka mutu lokacin da hasumiya a Silowam ya fāɗi a kansu, sun fi dukan sauran
mutanen Urushalima laifi ne? 5 Ina gaya muku, a'a! Amma in ba ku tuba ba, ku ma
duka za ku hallaka."
6 Sai ya ba su wannan misali ya ce, "Wani mutum yana da itacen ɓaure, da aka
shuka a gonar inabinsa. Da ya je cire 'ya'yan itacen, sai ya tarar ba tă yi 'ya'ya ba.
7 Sai ya ce wa mai lura da gonar inabin, 'Yau shekara uku ke nan ina zuwa neman
'ya'yan ɓaure daga itacen nan, amma ba na samun kome. Sare shi! Don me za a bar
shi ya tare wuri.'
8 "Mutumin ya amsa ya ce, 'Ranka yă daɗe, ka bar shi, in yi masa banƙasa, in kuma
zuba masa taki har na shekara ɗaya. 9 In kuwa ya ba da 'ya'ya shekara mai zuwa,
yana da kyau! In kuwa ba haka ba, sai ka sare shi.' "

### *Yesu ya warkar da mace gurguwa a ranar Asabbaci.*

10 Wata ranar Asabbaci, Yesu yana koyarwa a wata majami'a, 11 a wurin kuwa,
akwai wata mace wadda aljani ya gurgunta, har na shekaru goma sha takwas. Duk
ta tanƙware, ba ta ma iya miƙewa ko kaɗan. 12 Da Yesu ya gan ta, sai ya kirata
gaba, ya ce mata, "Mace, an 'yantar da ke daga rashin lafiyarki." 13 Sai ya ɗibiya
hannuwansa a kanta, nan da nan sai ta miƙe, ta yabi Allah.
14 Amma mai mulkin majami'ar ya ji haushi da Yesu ya yi warkarwa a ranar
Asabbaci. Sai ya ce wa mutanen, "Akwai ranaku shida da ya kamata a yi aiki. Saboda
haka, ku zo a ranakun nan a warkar da ku, ba ranar Asabbaci ba."
15 Ubangiji ya amsa masa ya ce, "Ku munafukai! Ashe, kowannenku ba yakan
kunce bijiminsa ko jakinsa, yă kai shi waje yă ba shi ruwa, a ranar Asabbaci ba?
16 Ashe, bai kamata a 'yantar da macen nan, diyar zuriyar Ibrahim, wadda Shaiɗan
ya daure, har shekara goma sha takwas, a ranar Asabbaci, daga abin da ya daure ta
ba?"
17 Sa'ad da ya faɗi wannan, sai duka masu gāba da shi suka kunyata. Amma mutane
kuwa suka yi murna saboda dukan abubuwan banmamaki da yake yi.

### *Misalai na ƙwayar mustad da na yisti*
### *(Mattiyu 13.31-33; Markus 4.30-32)*

18 Sai Yesu ya yi tambaya ya ce, "Yaya mulkin Allah yake? Da me zan kwatanta
shi? 19 Yana kama da ƙwayar mustad, wadda wani mutum ya ɗauka, kuma ya shuka
a gonarsa. Ta yi girma, ta zama itace, kuma tsuntsayen sararin sama suka huta a
rassansa."
20 Ya sāke tambaya, "Da me zan kwatanta mulkin Allah? 21 Yana kama da yisti
wadda mace ta ɗauka, ta kwaɓa garin alkama mai yawa da shi, har sai da yistin ya
gauraye kullun duka."

### *Matsattsiyar ƙofa*
### *(Mattiyu 7.13,14,21-23)*

22 Sa'ad da Yesu yana kan hanyarsa zuwa Urushalima, sai ya bi ta cikin garuruwan
da ƙauyukan, yana koyarwa. 23 Sai wani ya tambaye shi ya ce, "Ya Ubangiji, shin,
wai mutane kima ne kawai za su sami ceto?"

Ya ce musu, 24 "Ku yi matuƙar ƙoƙari ku shiga ta matsattsiyar ƙofa, domin ina faɗa
muku, mutane da yawa za su yi ƙoƙarin shiga, amma ba za su iya ba. 25 Da zaran
maigidan ya tashi ya rufe ƙofar, za ku tsaya a waje kuna ƙwanƙwasawa, kuna roƙo
cewa, 'Ranka yǎ daɗe, buɗe mana ƙofa.'

"Amma shi zai amma ya ce, 'Ni ban san ku, ko inda kuka fito ba.'

26 "Sa'an nan za ku ce, 'Haba, mu da muka ci, muka sha tare da kai, har ka yi
koyarwa a cikin titi-titi namu.'

27 "Amma shi zai amma ya ce, 'Ban san ku, ko inda kuka fito ba. Ku rabu da ni,
dukan ku masu aikata mugunta!'

28 "Za a yi kuka a can, da cizon haƙora, sa'ad da kuka ga Ibrahim, da Ishaku, da
Yaƙub, da dukan annabawa a mulkin Allah, amma ku kuwa, za a jefar da ku a waje.
29 Mutane za su zo daga gabas, da yamma, da kudu, da arewa, su ɗauki wuraren
zamansu a bikin, a cikin mulkin Allah. 30 Tabbatacce, akwai waɗansu da suke na
ƙarshe, da za su zama na farko, na farko kuma, da za su zama na ƙarshe."

### *Baƙin cikin Yesu domin Urushalima*
*(Mattiyu 23.37-39)*

31 A wannan lokaci, waɗansu Farisiyawa suka zo suka ce wa Yesu, "Ka bar nan ka
tafi wani wuri dabam. Hiridus yana so ya kashe ka."

32 Ya amsa ya ce, "Ku je ku gaya wa dilan nan, wato, mai makirci cewa, 'Da yau
da kuma gobe, zan fitar da aljanu, in kuma warkar da mutane, sa'an nan a rana ta
uku in cika burin aikina. 33 Duk da haka, dole in ci gaba da aikin a yau, da kuma
gobe, sa'an nan in ci gaba da yin haka kashegari kuma, gama tabbatacce, ba annabi
da yakan mutu a bayan birnin Urushalima!'

34 "Urushalima, ayya Urushalima, ke da kika kashe annabawa, kuma kika jefa wa
waɗanda aka aika gare ki da duwatsu. Sau da yawa na yi kewan in tattara 'ya'yanki
wuri ɗaya, kamar yadda kaza takan tattara 'ya'yanta cikin fikafikanta, amma ba ki
yarda ba! 35 Duba, an bar muku gidanku fanko. Ina kuwa faɗa muku, ba za ku sāke
ganina ba, sai kun ce, 'Mai albarka ne shi wanda yake zuwa cikin sunan Ubangiji.' "

## 14

### *Yesu a gidan Bafarisiye*

1 Wata ranar Asabbaci, da Yesu ya shiga gidan wani sanannen Bafarisiye don cin
abinci, sai mutane suka zuba masa ido da kyau. 2 A nan a gabansa kuwa akwai wani
mutum mai ciwon kumburin ƙafa da hannu. 3 Sai Yesu ya tambayi masanan dokoki
da Farisiyawa ya ce, "Daidai ne bisa ga doka, a yi warkarwa a ranar Asabbaci, ko
babu?" 4 Amma ba su ce kome ba. Sai ya riƙe mutumin, ya warkar da shi, sa'an nan
ya sallame shi.

5 Sai ya tambaye, su ya ce, "In wani a cikinku yana da ɗa, ko bijimi da ya faɗa a
rijiya a ranar Asabbaci, ba za ku cire shi nan da nan ba?" 6 Suka rasa abin faɗi.

7 Da ya lura da yadda baƙi suna zaɓan wuraren zama masu bangirma a tebur, sai
ya faɗa musu wannan misali, ya ce; 8 "In wani ya gayyace ka bikin aure, kada ka
zaɓi wurin zama mai bangirma, don wataƙila akwai wani da ya fi ka girma, da aka
gayyata. 9 In kuwa haka ne, wanda ya gayyace duk biyunku, zai zo ya ce maka, 'Ka ba
wa mutumin nan wurin zamanka.' Ka ga, an ƙasƙantar da kai, kuma dole ka ɗauki
wuri mafi ƙasƙanci. 10 Amma in an gayyace ka, ɗauki wuri mafi ƙasƙanci, don in
wanda ya gayyace ka ya zo, zai ce maka, 'Ka hawo nan aboki a wuri mafi girma.'

Wannan zai ɗaukaka ka a gaban dukan ʼyanʼuwanka baƙi. 11 Gama duk wanda ya
ɗaukaka kansa, za a ƙasƙantar da shi. Shi wanda kuma ya ƙasƙantar da kansa, za
a ɗaukaka shi."
12 Sai Yesu ya ce wa wanda ya gayyace shi, "Lokacin da ka shirya biki ko liyafa, kada
ka gayyaci abokanka, ko ʼyanʼuwanka, ko danginka, ko kuma maƙwabtanka masu
arziki, gama in ka yi haka, suna iya gayyatarka, su biya maka alherin da ka yi musu.
13 Amma lokacin da ka kira biki, ka gayyaci matalauta, da guragu, da shanyayyu, da
makafi. 14 Ta haka, za ka sami albarka. Ko da yake ba za su iya biyan ka ba, za a
biya ka a ranar tashin masu adalci daga matattu."

*Misalin babban biki*
*(Mattiyu 23.37-39)*

15 Da jin haka, sai wani da yake tare da shi a tebur ɗin, ya ce wa Yesu, "Mai albarka
ne wanda zai ci abinci a bikin nan a mulkin Allah."
16 Yesu ya amsa ya ce, "Wani mutum yana shirya wani babban biki, ya kuma gayyaci
baƙi da yawa. 17 Da lokacin bikin ya yi, sai ya aiki bawansa ya je ya ce wa waɗanda
aka gayyata, ʻKu zo, don an shirya kome.ʼ
18 "Amma sai dukansu suka fara ba da hujjoji. Na farkon ya ce, ʻNa sayi gona
yanzun nan, dole in je in ga yadda take, ina roƙonka ka yi mini haƙuri.ʼ
19 "Wani ya ce, ʻNa sayi shanun noma guda goma yanzun nan, ina kan hanyata ke
nan in gwada su, ina roƙonka, ka yi mini haƙuri.ʼ
20 "Har yanzu wani ya ce, ʻNa yi aure yanzun nan, don haka ni ba zan iya zuwa
ba.ʼ
21 "Bawansa ya dawo ya gaya wa maigidansa wannan. Sai maigidan ya yi fushi,
ya ba da umarni ga bawansa ya ce, ʻKa fita da sauri, ka bi titi-titi da lungu-lungu na
garin, ka kawo matalauta, da guragu, da makafi, da shanyayyu.ʼ
22 "Bawan ya dawo ya ce, ʻRanka yǎ daɗe, an yi abin da ka umarta, amma har
yanzu da sauran wuri.ʼ
23 "Maigidan ya ce wa bawansa, ʻKa je kan hanyoyin da layi-layi na karkara, ka sa
su shigo, don gidana ya cika.ʼ 24 Ina gaya muku, babu ko ɗaya daga cikin mutanen
nan da aka gayyata da zai ɗanɗana bikina."

*Wahalar rayuwar almajiri*
*(Mattiyu 10.37,38)*

25 Taron mutane mai yawa suna tafiya tare da Yesu, sai ya juya ya ce musu, 26 "Duk
wanda yakan zo wurina, amma bai ƙi mahaifinsa da mahaifiyarsa, da matarsa da
ʼyaʼyansa, da ʼyanʼuwansa mata da maza, kai, har ma ransa ba, ba zai iya zama
almajirina ba. 27 Kuma duk wanda ba yakan ɗauki gicciyensa ya bi ni ba, ba zai iya
zama almajirina ba.
28 "In wani daga cikinku yana so ya gina gidan sama, ai, yakan fara zama ne, ya yi
lissafin abin da ginin zai ci tukuna, don yǎ ga ko yana da isashen kuɗi da zai gama
ginin. 29 Gama in ya sa tushen gini, amma bai iya gamawa ba, duk wanda ya gani zai
yi masa baʼa, 30 yana cewa, ʻWannan mutum ya fara gini, amma bai iya gamawa ba.ʼ
31 "Ko kuma, wane sarki ne, in zai je yaƙi da wani sarki, ai, yakan fara zama ne,
ya duba ya ga, ko da mutane dubu goma, shi zai iya ƙarawa da mai zuwa da dubu
ashirin? 32 In ba zai iya ba, to, tun suna nesa, zai aika da wakilai, su je neman
sharuɗan salama. 33 Haka nan fa, kowane ne a cikinku, da ba ya rabu da abin da
yake da shi ba, ba zai iya zama almajirina ba.

*(Mattiyu 5.13; Markus 9.50)*

34 "Gishiri fa yana da kyau, amma in gishiri ya rabu da daɗin ɗanɗanonsa, ta yaya
za a sāke mai da daɗin ɗanɗanonsa? 35 Ba shi da wani amfani, ko ga ƙasa, ko ga
juji, sai dai a zubar da shi.

"Duk mai kunnen ji, yă ji."

# 15

*Misalin ɓatacciyar tunkiya*
*(Mattiyu 18.12-14)*

1 Yanzu fa, masu karɓar haraji da "masu zunubi" duka suna taruwa don jin
koyarwar Yesu. 2 Amma Farisiyawa da malaman dokoki suka yi gunaguni, suna cewa,
"Wannan mutum yana karɓan 'masu zunubi,' kuma yana ci tare da su."
3 Sai Yesu ya faɗa musu wannan misali ya ce, 4 "In ɗayanku yana da tumaki ɗari,
sa'an nan ɗayansu ta ɓace. Ashe, ba zai bar tasa'in da tara a fili ya je neman wadda
ta ɓace, har sai ya same ta ba? 5 In ya same ta, zai sa ta a kafaɗa da murna, 6 ya
dawo gida. Sa'an nan zai kira abokansa da maƙwabtansa wuri ɗaya ya ce, 'Ku taya
ni murna, na sami tunkiyana da ta ɓata.' 7 Ina gaya muku, haka za a yi murna sosai
a sama, a kan mai zunubi guda ɗaya da ya tuba, fiye da masu adalci tasa'in da tara,
waɗanda ba su bukatan tuba.

*Misalin kuɗi da ya ɓace*

8 "Ko kuwa in wata mace tana da kuɗi na azurfa guda goma, sa'an nan ɗaya ya
ɓata, ashe, ba za tă ƙuna fitila, ta share gidan, ta nema a hankali, har sai ta samu ba?
9 In ta same shi, sai ta kira ƙawayenta da maƙwabtanta wuri ɗaya, ta ce musu, 'Ku
taya ni murna, na sami kuɗina da ya ɓata.' 10 Haka, ina gaya muku, akwai murna a
gaban mala'ikun Allah a kan mai zunubi guda ɗaya, da ya tuba."

*Misalin ɗa da ya ɓace*

11 Yesu ya ci gaba da cewa, "Akwai wani mutum wanda yake da 'ya'ya biyu maza.
12 Karamin ya ce wa mahaifinsu, 'Baba, ba ni rabon gādona.' Sai mahaifin ya raba
musu dukiyarsa.
13 "Bayan 'yan kwanaki, sai ƙaramin ɗan ya tattara kayansa duk, ya tashi ya tafi
wata ƙasa mai nisa. A can, ya ɓatar da dukiyarsa duka a rayuwar banza. 14 Bayan
ya ɓatar da kome, sai ga muguwar yunwa a dukan ƙasar, har ya shiga rashi. 15 Sai
ya je ya sami aiki a wurin wani mutumin ƙasar, wanda ya aike shi a gonakinsa, ya
yi kiwon aladu. 16 Ya yi marmarin cin dusan da aladun suke ci, amma ba wanda ya
ba shi wani abu.
17 "Da hankalinsa ya dawo, sai ya ce, 'Kai, bayin mahaifina guda nawa ne, da suke
da abinci fiye da isashe, ni kuma ina nan, zan mutu don yunwa! 18 Zan tashi in koma
wurin mahaifina, in ce masa, "Baba, na yi wa sama, na kuma yi maka zunubi. 19 Ni
ban isa a ƙara kira na ɗanka ba. Ka mai da ni kamar ɗaya daga cikin bayinka." '
20 Sai ya tashi ya kama hanya ya koma wurin mahaifinsa.

"Amma tun yana nesa, mahaifinsa ya hange shi. Tausayi kuma ya kama shi, sai ya tashi ya ruga da gudu wurinsa, ya rungume shi, ya yi masa sumba.

21 "Sai ɗan ya ce masa, 'Baba, na yi wa sama, na kuma yi maka zunubi. Ni ban isa
a ƙara kira na ɗanka ba.'
22 "Amma mahaifin ya ce wa bayinsa, 'Maza! Ku kawo riga mafi kyau ku sa masa.
Ku sa zobe a yatsarsa, da takalma kuma a ƙafafunsa. 23 Ku kawo ɗan saniya mai
ƙiba ku yanka. Bari mu yi biki mu yi shagali. 24 Gama ɗan nan nawa, da ya mutu,
amma yanzu yana da rai kuma. Da ya ɓata, amma yanzu an same shi.' Sai suka fara
shagali.
25 "Yayinda ake haka, babban ɗan yana gona. Da ya zo kusa da gida, sai ya ji ana
kiɗi ana rawa. 26 Sai ya kira ɗaya daga cikin bayin, ya tambaye shi abin da yake
faruwa. 27 Bawan ya ce, 'Ai, ɗan'uwanka ne ya dawo, shi ne mahaifinka ya yanka

ɗan saniya mai ƙiba, gama ya yi murna ya karɓi ɗansa da ya dawo gida lafiyayye,
ba abin da ya same shi.'
[28] "Sai yayan ya yi fushi, ya ƙi shiga gida. Sai mahaifinsa ya fita ya roƙe shi.
[29] Amma ya amsa wa mahaifinsa ya ce, 'Duba! Duk waɗannan shekaru, ina yin
maka aiki kamar bawa, ban taɓa maka rashin biyayya ba. Duk da haka, ba ka taɓa
ba ni ko ɗan akuya domin in yi shagali da abokaina ba. [30] Amma da wannan ɗan
naka, wanda ya ɓatar da dukiyarka a kan karuwai ya dawo, ka yanka masa ɗan
saniya mai ƙiba!'
[31] "Sai mahaifin ya ce masa, 'Ɗana, kullum kana nan tare da ni, kuma duk abin
da nake da shi, naka ne. [32] Amma ya zama mana dole, mu yi shagali, mu yi murna,
domin ɗan'uwan nan naka, da ya mutu, yanzu kuwa yana da rai, da ya ɓata, amma
yanzu an same shi.' "

# 16

*Misalin manaja mai wayo*

[1] Yesu ya ce wa almajiransa, "An yi wani mai arziki wanda aka yi wa manajansa
zargin yin banza da dukiyarsa. [2] Sai ya kira manajan, ya tambaye shi, 'Me nake ji
haka a kanka? Ka kawo lissafin aikinka, domin ba za ka iya cin gaba da aikinka ba.'
[3] "Sai manajan ya ce cikin tunaninsa, 'Maigidana zai kore ni daga aiki, me zan yi?
Ba ni da ƙarfin noma, kuma ina jin kunyan yin bara. [4] Na san abin da zan yi, don
mutane su karɓe ni a gidajensu, bayan an kore ni daga aiki a nan.'
[5] "Sai ya kira kowane ɗaya da maigidansa yake bin bashi. Ya tambayi na farkon ya
ce, 'Nawa ne maigidana yake bin ka?'
[6] "Ya amsa ya ce, 'Garwar mai na zaitun guda ɗari tara.'
"Manajan ya ce, 'Ga takardarka, ka zauna maza ka mai da shi ɗari huɗu.'
[7] "Ya kuma tambayi na biyun, 'Kai fa, nawa ne ake bin ka?'
"Sai ya amsa ya ce, 'Buhunan alkama dubu.'
"Ya ce, 'Ga takardarka, ka mai da shi ɗari takwas.'
[8] "Maigidan kuwa ya yabi manajan nan marar gaskiya saboda wayonsa. Gama
'yan duniyan nan suna da wayon yin hulɗa da junansu fiye da 'yan haske. [9] Ina gaya
muku, ku yi amfani da dukiya na wannan duniya, domin ku sami wa kanku abokai.
Saboda bayan dukiyar ta ƙare, za a karɓe ku a wuraren zama da sun dawwama.
[10] "Duk wanda ana amincewa da shi cikin ƙaramin abu, ana kuma amincewa da
shi cikin babba. Kuma duk marar gaskiya cikin ƙaramin abu, zai zama marar gaskiya
cikin babba. [11] In fa ku ba amintattu ne cikin tafiyar da dukiya ta wannan duniya ba,
wa zai amince muku da dukiya ta gaskiya? [12] In fa ku ba amintattu ne cikin tafiyar
da dukiyar wani ba, wa zai ba ku dukiya naku, na kanku?
[13] "Babu wani bawa mai iya bauta wa iyayengiji biyu ba. Ko dai ya ƙi ɗaya, ya so
ɗayan, ko kuwa ya dāge ga yi wa ɗaya bauta, sa'an nan ya rena ɗayan. Ba za ku iya
ku bauta wa Allah tare da bauta wa Mammon (wato, Kuɗi) a lokaci ɗaya ba."

*(Mattiyu 11.12,13; 5.31,32; Markus 10.11,12)*

[14] Da Farisiyawa masu son kuɗi suka ji wannan duka, sai suka yi wa Yesu tsaki.
[15] Ya ce musu, "Ku ne masu mai da kanku marasa laifi a gaban mutane, amma Allah
ya san zuciyarku. Abu mai daraja a gaban mutane, abin ƙyama ne a gaban Allah.

*Karin koyarwa*

[16] "An yi shelar Doka da Annabawa har zuwa lokacin Yohanna. Tun daga lokacin
nan, bisharar mulkin Allah ne ake wa'azinta, kowa kuma yana ƙoƙarin kutsa kai ya
shiga. [17] Gama ta fi sauƙi sama da ƙasa su shuɗe, da a ce ɗigo guda ɗaya na rubutun,
ya fita ya fāɗi daga cikin Doka.

18 "Duk wanda ya saki matarsa ya auri wata mace, zina ne yake yi. Kuma mutumin da ya auri macen da aka sake, zina ne yake yi.

### *Mai arziki da Lazarus*

19 "An yi wani mutum mai arziki wanda yakan sa tufafi masu ruwan shunayya, da kuma na lallausan lilin, yana kuma cikin rayuwar jin daɗi kullum. 20 A ƙofar gidansa kuma akan ajiye wani mai bara, mai suna Lazarus, wanda jikinsa duk gyambuna ne.
21 Shi kuwa yakan yi marmarin cin abin da yakan fāɗi daga tebur na mai arzikin nan. Har karnuka ma sukan zo su lashe gyambunansa.

22 "Ana nan, sai mai baran ya mutu, kuma mala'iku suka ɗauke shi zuwa gefen Ibrahim. Mai arzikin ma ya mutu, aka kuma binne shi. 23 A cikin jahannama ta wuta, inda yana shan azaba, ya ɗaga kai ya hangi Ibrahim can nesa, da kuma Lazarus a gefensa. 24 Sai ya yi masa kira ya ce, 'Baba, Ibrahim, ka ji tausayina, ka aiki Lazarus ya sa ɗan yatsarsa a ruwa, ya ɗiga mini a harshe saboda in ji sanyi, domin ina shan azaba cikin wannan wuta.'

25 "Amma Ibrahim ya ce, 'Ka tuna fa ɗana, a lokacin da kake duniya, ka sami abubuwa masu kyau naka, Lazarus kuwa ya sami munanan abubuwa. Amma yanzu ya sami ta'aziyya a nan, kai kuwa kana shan azaba. 26 Ban da wannan duka ma, tsakaninmu da kai, akwai wani babban rami da aka yi, yadda waɗanda suke son ƙetarewa daga nan zuwa wurinku, ba za su iya ba, kuma ba mai iya ƙetarewa daga wurinku zuwa wurinmu.'

27 "Ya amsa ya ce, 'To, ina roƙonka, ya uba, ka aiki Lazarus zuwa gidan mahaifina,
28 gama ina da 'yan'uwana biyar maza. Bari yă ba su gargaɗi, don kada su ma su zo wurin nan mai azaba.'

29 "Ibrahim ya amsa ya ce, 'Suna da Musa da Annabawa, ai, sai su saurare su.'

30 "Sai ya ce, 'A'a, ya uba, Ibrahim, in dai wani ya tashi daga matattu ya je wurinsu, za su tuba.'

31 "Amma ya ce masa, 'In ba su saurari Musa da Annabawa ba, kai, ko da wani ya tashi daga matattu ma, ba za su saurare shi ba.' "

## 17

### *Zunubi, bangaskiya da aiki*
### *(Mattiyu 18.6,7,21,22; Markus 9.42)*

1 Yesu ya ce wa almajiransa, "Dole ne a sami abubuwan da suke sa mutane su yi zunubi, amma kaiton mutumin nan wanda suke zuwa ta wurinsa. 2 Gwamma a ɗaura dutsen niƙa a wuyansa, a jefa shi cikin teku, da ya sa ɗaya daga cikin ƙananan yaran nan ya yi zunubi. 3 Saboda haka, ku lura da kanku.

"In ɗan'uwanka ya yi zunubi, ka kwaɓe shi. In ya tuba, ka gafarta masa. 4 In ya yi maka laifi sau bakwai a rana ɗaya, ya kuma dawo sau bakwai ɗin a wurinka, yana cewa, 'Na tuba,' sai ka gafarta masa."

5 Sai manzannin suka ce wa Ubangiji, "Ka ƙara mana bangaskiya!"

6 Ya amsa musu ya ce, "In kuna da bangaskiya da take ƙanƙani kamar ƙwayar mustad, kuna iya ce wa wannan itacen durumi, 'Ka tumɓuke daga nan, ka dasu a cikin teku.' Zai kuwa yi muku biyayya.

7 "In ɗaya a cikinku yana da bawa, wanda yake masa noma, ko kiwon tumaki, da dawowar bawan daga gonar, ai, ba zai ce masa, 'Ka zo nan, ka zauna, ka ci abinci ba'? 8 Ashe, ba zai ce masa, 'Ka shirya mini abincin yamma, ka shirya ka yi mini hidima domin in ci in sha, bayan haka kana iya ci, ka kuma sha ba'? 9 Shin, zai gode wa bawan don yă yi aikin da aka ce ya yi ne? 10 Haka ku ma, bayan kun yi duk abin da aka ce muku ku yi, ya kamata ku ce, 'Mu bayi ne marasa cancanta, mun dai yi aikinmu ne kaɗai.' "

### *An warkar da kutare goma*

11 Yesu yana kan hanyarsa zuwa Urushalima, sai ya bi takan iyakar Samariya da
Galili. 12 Da zai shiga wani ƙauye, sai maza goma da suke da kuturta suka sadu da
shi. Suka tsaya da nesa, 13 suka yi kira da babbar murya, suka ce, “Yesu, Ubangiji, ka
ji tausayinmu!”
14 Da ya gan su sai ya ce, “Ku je ku nuna kanku ga firistoci.” Suna kan hanyar tafiya
sai suka tsabtacce.
15 Da ɗayansu ya ga ya warke, sai ya koma, yana yabon Allah da babbar murya.
16 Ya zo ya fāɗi a gaban Yesu, ya gode masa. Shi kuwa mutumin Samariya ne.
17 Yesu ya yi tambaya ya ce, “Ba duka goma ne aka tsabtacce ba? Ina sauran taran?
18 Ba wanda ya dawo don yǎ yabi Allah, sai dai wannan baƙon?” 19 Sai ya ce masa,
“Tashi, ka yi tafiyarka, bangaskiyarka ta warkar da kai.”

### *Zuwan mulkin Allah*
*(Mattiyu 24.23-28,37-41)*

20 Wata rana, Farisiyawa suka tambaye shi lokacin da mulkin Allah zai zo, Yesu ya
amsa ya ce, “Ai, mulkin Allah ba takan zo ta wurin yin kallon ku ba. 21 Mutane kuma
ba za su ce, ‘Ga shi nan,’ ko kuma, ‘Ga shi can’ ba, domin mulkin Allah yana cikinku
ne.”
22 Sai ya ce wa almajiransa, “Lokaci yana zuwa da za ku yi marmarin ganin rana
ɗaya cikin ranakun Ɗan Mutum, amma ba za ku gani ba. 23 Mutane za su ce muku,
‘Ga shi can!’ Ko kuma, ‘Ga shi nan!’ Kada ku yi hanzarin binsu. 24 Gama Ɗan Mutum,
a cikin ranarsa, zai zama kamar walƙiya da take walƙawa, da take kuma haskaka
sararin sama, daga wannan kusurwa zuwa wancan kusurwa. 25 Amma da fari, dole
yǎ sha wahaloli masu yawa, kuma mutanen zamanin nan su ƙi shi.
26 “Daidai kamar yadda ya faru a zamanin Nuhu, haka zai zama a zamanin Ɗan
Mutum. 27 Mutane suna ci, suna sha, suna aurayya, ana kuma ba da su ga aure, har
ranar da Nuhu ya shiga jirgin. Sa’an nan ambaliyar ruwan ya sauka, ya hallaka su
duka.
28 “Haka ma aka yi a zamanin Lot. Mutane suna ci, suna sha, suna saya, suna
sayarwa, suna shuki, suna kuma gine-gine. 29 Amma a ranar da Lot ya bar Sodom,
sai aka yi ruwan wuta da farar wuta daga sama, aka hallaka su duka.
30 “Daidai haka zai zama, a ranar da Ɗan Mutum zai bayyana. 31 A ranan nan,
kada wanda yake kan rufin gidansa ya sauka don yǎ kwashe dukiyarsa da take cikin
gidan. Haka ma duk wanda yake gona, kada yǎ koma don wani abu. 32 Ku tuna fa
da matar Lot! 33 Duk wanda yake so ya ceci ransa, zai rasa shi, amma duk wanda ya
rasa ransa, zai cece shi. 34 Ina gaya muku, a daren nan, mutane biyu za su kasance
a gado ɗaya, za a ɗauki ɗaya, a bar ɗayan. 35 Mata biyu za su kasance suna niƙan
hatsi tare, za a ɗauki ɗaya, a bar ɗayan.”*
37 Suka tambaya, suka ce, “A ina ne, ya Ubangiji?”
Ya ce musu, “Ai, inda gawa take, nan ne ungulai za su taru.”

## 18

### *Misalin gwauruwa mai naciya*

1 Yesu ya ba wa almajiransa wani misali, don yǎ koya musu yadda ya kamata su
dinga yin addu’a kullum, ban da fasawa. 2 Ya ce, “A wani gari, an yi wani alƙali
wanda ba ya tsoron Allah, bai kuma kula da mutane ba. 3 A garin nan kuma, akwai
wata gwauruwa, wadda ta dinga zuwa wurin alƙalin nan, da roƙo cewa, ‘Ka yi mini
adalci tsakanina da maƙiyina.’

* **17:35** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da bar. 36 Mutum biyu za su kasance a gona, a ɗau ɗaya, a bar ɗaya.

4 “An daɗe yana ƙi, amma a ƙarshe ya ce cikin tunaninsa, ‘Ko da yake ba na tsoron
Allah, ba na kuma kula da mutane ba, 5 amma don gwauruwan nan ta dame ni, zan
tabbatar cewa ta sami adalci, domin kada tă gajiyar da ni, da yawan zuwanta.’ ”
6 Sai Ubangiji ya ce, “Ku ji fa abin da alƙalin nan, marar gaskiya, ya ce. 7 Ashe,
Allah ba zai biya wa zaɓaɓɓunsa da suke masa kuka, dare da rana adalci ba? Zai ci
gaba da ƙin sauraronsu ne? 8 Ina gaya muku, zai tabbatar sun sami adalci, ban da
ɓatan lokaci. Amma sa’ad da Ɗan Mutum ya dawo, zai sami bangaskiya a duniya ke
nan?”

### *Misalin Bafarisiye da mai karɓar haraji*

9 Yesu ya kuma faɗi wannan misali ga waɗansu masu taƙama da adalcinsu, kuma
suna rena sauran mutane ya ce, 10 “Waɗansu mutane biyu sun tafi haikali don yin
addu’a. Ɗaya Bafarisiye ne, ɗayan kuma mai karɓar haraji. 11 Sai Bafarisiyen ya
tashi tsaye, ya yi addu’a game da kansa yana cewa, ‘Allah, na gode maka, saboda ni
ba kamar sauran mutane ba ne, wato, mafasa, masu aikata mugunta, masu zina, ko
kuma kamar mai karɓar harajin nan. 12 Ina azumi sau biyu a mako, ina ba da zakka
daga kowane abin da na samu.’
13 “Amma mai karɓar harajin ya tsaya daga nesa. Bai ma iya ɗaga kansa sama ba,
sai ya buga ƙirjinsa, yana cewa, ‘Allah, ka yi mini jinƙai, ni mai zunubi ne.’
14 “Ina gaya muku, wannan mutum ne, ba ɗayan ba, ya koma gida baratacce, babu
laifi a gaban Allah. Gama duk wanda ya ɗaukaka kansa, za a ƙasƙantar da shi.
Wanda kuma ya ƙasƙantar da kansa, za a ɗaukaka shi.”

### *Yesu da ƙananan yara*
### *(Mattiyu 19.13-15; Markus 10.13-16)*

15 Mutane suna kawo jarirai wurin Yesu don yă taɓa su. Da almajiransa suka ga
haka, sai suka kwaɓe su. 16 Amma Yesu ya kira yaran a wurinsa ya ce, “Ku bar yara
ƙanana su zo wurina. Kada ku hana su, gama mulkin Allah na irin waɗannan ne.
17 Gaskiya nake gaya muku, duk wanda ba zai karɓi mulkin Allah kamar ƙaramin
yaro ba, ba zai taɓa shiga mulkin ba.”

### *Mai mulki mai arziki*
### *(Mattiyu 19.16-30; Markus 10.17-31)*

18 Wani mai mulki ya tambayi Yesu ya ce, “Malam managarci, me zan yi don in gāji
rai madawwami?”
19 Yesu ya amsa ya ce, “Don me kake kira na managarci? Ai, ba wani nagari, sai
Allah kaɗai. 20 Ka san dokokin da suka ce, ‘Kada ka yi zina, kada ka yi kisankai, kada
ka yi sata, kada ka ba da shaida ta ƙarya, ka girmama mahaifinka da mahaifiyarka.’ ”
21 Mutumin ya ce, “Ai, tun ina ƙarami, na kiyaye duka waɗannan.”
22 Da Yesu ya ji haka, sai ya ce masa, “Akwai abu ɗaya har yanzu da ya rage maka.
Ka sayar da duk abin da kake da shi, ka ba wa matalauta, sa’an nan za ka sami dukiya
a sama. Bayan haka, ka zo ka bi ni.”
23 Da jin haka, sai ya ɓata rai, domin shi mai arziki ne sosai. 24 Yesu ya kalle shi ya
ce, “Yana da wuya fa, masu arziki su shiga mulkin Allah! 25 Tabbatacce, zai fi sauƙi
raƙumi ya shiga ta kafar allura, da mai arziki ya shiga mulkin Allah.”
26 Waɗanda suka ji wannan suka yi tambaya suka ce, “To, wa zai iya samun ceto?”
27 Yesu ya amsa ya ce, “Abin da ba ya yiwuwa ga mutane, mai yiwuwa ne ga Allah.”
28 Sai Bitrus ya ce, masa, “To, ga shi mun bar kome da muke da shi, don mu bi ka!”
29 Yesu ya ce musu, “Gaskiya nake gaya muku, ba wanda ya bar gida, ko mata, ko
’yan’uwa maza, ko iyaye, ko yara, saboda mulkin Allah, 30 da zai kāsa samun riɓi
mai yawa, a wannan zamani, ya kuma sami rai madawwami a zamani mai zuwa.”

### *Yesu ya sāke magana a kan mutuwarsa*
### *(Mattiyu 20.17-19; Markus 10.32-34)*

31 Sai ya kai Sha Biyun gefe ɗaya, ya ce musu, “Za mu Urushalima, kuma dukan abin
da annabawa suka rubuta a kan Ɗan Mutum zai cika. 32 Za a ba da shi ga Al’ummai,
za su yi masa ba’a, su zage shi, su tofa masa miyau, 33 za su yi masa bulala, su kuma
kashe shi. A rana ta uku kuma zai tashi.”
34 Almajiran ba su gane da ko ɗaya daga cikin wannan ba. An ɓoye musu
ma’anarsa, kuma ba su gane da abin da yake magana a kai ba.

### *Makaho mai bara ya sami ganin gari*
### *(Mattiyu 20.17-19; Markus 10.32-34)*

35 Da Yesu ya yi kusa da Yeriko, akwai wani makaho da yake zaune a gefen hanya,
yana bara. 36 Da ya ji taron suna wucewa, sai ya yi tambaya ko mene ne ke faruwa.
37 Suka ce masa, “Ai, Yesu Banazare ne ke wucewa.”
38 Sai ya yi kira ya ce, “Yesu, Ɗan Dawuda, ka yi mini jinƙai!”
39 Mutane da suke gaba suka kwaɓe shi, suka ce masa ya yi shiru. Amma sai ya
ƙara ɗaga murya, yana cewa, “Ɗan Dawuda, ka yi mini jinƙai!”
40 Sai Yesu ya tsaya, ya ba da umarni a kawo mutumin wurinsa. Da ya zo kusa,
Yesu ya tambaye shi ya ce, 41 “Me kake so in yi maka?”
Sai ya amsa ya ce, “Ubangiji, ina so in sami ganin gari.”
42 Yesu ya ce masa, “Ka sami ganin garinka; bangaskiyarka ta warkar da kai.”
43 Nan da nan, ya sami ganin garinsa, kuma ya bi Yesu, yana yabon Allah. Da dukan
mutane suka ga wannan, sai su ma suka yabi Allah.

# 19

### *Zakka mai karɓar haraji*

1 Yesu ya shiga Yeriko, yana ratsa ta cikinta. 2 Akwai wani mutum a garin, mai suna
Zakka. Shi shugaban masu karɓar haraji ne, mai arziki kuma. 3 Ya so yǎ ga ko wane
ne Yesu, amma saboda taron, bai iya ba, domin shi gajere ne. 4 Saboda haka, ya yi
gaba da gudu, kuma ya hau itacen sikamo, don yǎ gan shi, tun da Yesu zai bi wannan
hanyar ne.
5 Da Yesu ya iso wurin, sai ya ɗaga ido sama, ya ce masa, “Zakka, ka yi maza ka
sauka. Ni kam, dole in sauka a gidanka yau.” 6 Sai ya sauka nan da nan, ya karɓe
shi da murna.
7 Dukan mutane suka ga haka, kuma suka fara gunaguni, suka ce, “Ya je don yǎ
zama baƙon ‘mai zunubi.’ ”
8 Amma Zakka ya tashi a tsaye, ya ce wa Ubangiji, “Duba, Ubangiji! Nan take, rabin
dukiyar da nake da shi, na ba wa matalauta. In kuma na taɓa cutan wani, a kan wani
abu, zan mayar da shi ninki huɗu.”
9 Sai Yesu ya ce masa, “Yau, ceto ya zo gidan nan, domin wannan mutum shi ma
ɗan Ibrahim ne. 10 Saboda Ɗan Mutum ya zo ne, domin yǎ nemi abin da ya ɓata, yǎ
cece shi kuma.”

### *Misalin mina goma*
### *(Mattiyu 25.14-30)*

11 Yayinda suna cikin sauraron wannan, sai ya ci gaba da gaya musu wani misali,
domin ya yi kusa da Urushalima, kuma mutanen suna tsammani mulkin Allah zai
bayyana, nan da nan. 12 Ya ce, “Wani mutum mai martaba ya tafi wata ƙasa mai nisa
don a naɗa shi sarki sa’an nan ya dawo. 13 Saboda haka ya kira bayinsa goma ya ba
su mina goma. Ya ce, ‘Ku yi kasuwanci da kuɗin nan, sai na dawo.’

14 “Amma talakawansa suka ƙi shi, sai suka aikar da wakilai bayansa, domin su ce,
‘Ba mu son wannan mutum ya zama sarkinmu.’
15 “Duk da haka, aka naɗa shi sarki, sa’an nan ya dawo gida. Sai ya aika aka kira
bayin da ya ba su kuɗin, don yă san ribar da suka samu.
16 “Na fari ya zo ya ce, ‘Ranka yă daɗe, minarka ya sami ribar goma.’
17 “Maigidan ya amsa ya ce, ‘Madalla, bawana mai kirki! Tun da ka yi aminci a
kan abu ƙanƙani, ka yi riƙon birane goma.’
18 “Na biyun ya zo ya ce, ‘Ranka yă daɗe, minarka ya sami ribar biyar.’
19 “Maigidansa ya ce, ‘Kai ka yi riƙon birane biyar.’
20 “Sai wani bawan ya zo ya ce, ‘Ranka yă daɗe, ga minarka. Na ɓoye shi a wani
ɗan tsumma. 21 Na ji tsoronka, don kai mai wuyan sha’ani ne. Kakan ɗauki abin da
ba ka ajiye ba, kakan kuma yi girbin abin da ba ka shuka ba.’
22 “Sai maigidansa, ya amsa ya ce, ‘Zan hukunta ka a kan kalmominka, kai mugun
bawa! Ashe, ka san cewa ni mai wuyan sha’ani ne, nakan ɗauka abin da ban ajiye
ba, ina kuma girbin abin da ban shuka ba? 23 Don me ba ka sa kuɗina a wajen ajiya,
don in na dawo, in sami riba a kai ba?’
24 “Sai ya ce wa waɗanda suke tsaye a wajen, ‘Ku karɓi minarsa ku ba wa wanda
yake da mina goma.’
25 “Suka ce, ‘Ranka yă daɗe, ai, yana da guda goma ko!’
26 “Ya amsa ya ce, ‘Ina gaya muku, duk wanda yake da abu, za a ƙara masa. Amma
wanda ba shi da shi kuwa, ko abin da yake da shi ma, za a karɓe. 27 Amma waɗannan
abokan gābana, waɗanda ba su so in zama sarkinsu ba, ku kawo su nan, ku karkashe
su, a gabana.’ ”

### *Shiga mai nasara*
### *(Mattiyu 21.1-11; Markus 11.1-11; Yohanna 12.12-19)*

28 Bayan Yesu ya yi wannan magana, sai ya yi gaba zuwa Urushalima. 29 Da ya kai
kusa da Betfaji da Betani, a tudun da ake kira Dutsen Zaitun, sai ya aiki almajiransa
guda biyu, ya ce musu, 30 “Ku je ƙauyen da yake gaba da ku. Da kuna shiga, za ku
tarar da wani ɗan jaki, wadda ba wanda ya taɓa hawa, a daure a wurin. Ku kunce
shi ku kawo nan. 31 In wani ya tambaye ku, ‘Don me kuke kunce shi?’ Ku ce masa,
‘Ubangiji yana bukatarsa.’ ”
32 Waɗanda aka aika su yi gaba suka tafi, suka kuwa tarar kamar yadda ya gaya
musu. 33 Suna cikin kunce ɗan jakin, sai masu ɗan jakin suka ce musu, “Don me
kuke kunce shi?”
34 Suka amsa suka ce, “Ubangiji ne na bukatarsa.”
35 Suka kawo shi wurin Yesu. Suka sa rigunarsu a kan ɗan jakin, sa’an nan suka
sa Yesu a kai. 36 Yana cikin tafiya, sai mutane suka shimfiɗa rigunarsu a kan hanya.
37 Da ya yi kusa da wurin da hanyar ta gangara zuwa Dutsen Zaitun, sai dukan
taron almajirai suka fara yabon Allah, da muryoyi masu ƙarfi, da murna, saboda
dukan ayyukan banmamaki da suka gani. Suna cewa,
38 “Mai albarka ne sarki wanda yake zuwa cikin sunan Ubangiji!”

“Salama ta kasance a sama, da ɗaukaka kuma a can cikin sama!”
39 Sai waɗansu Farisiyawa a cikin taron suka ce wa Yesu, “Malam, ka kwaɓi
almajiranka!”
40 Ya amsa ya ce, “Ina gaya muku, ko da sun yi shiru, duwatsu za su fara kirari.”
41 Da ya yi kusa da Urushalima, ya kuma ga birnin, sai ya yi kuka a kanta, 42 kuma
ya ce, “In ke, ko ke ɗin ma, dā ma kin san abin da zai kawo miki salama a wannan
rana, amma yanzu an ɓoye shi daga idanunki. 43 Ranakun za su auko miki, a lokacin
da abokan gābanki za su gina bango gāba da ke, su kuma kewaye inda kike, za su

kuma tsare kowane gefenki, su sa ke a tsakiya. 44 Za su fyaɗa ke a ƙasa, ke da ’ya’yan
da suke cikin katanganki. Ba za su bar wani dutse a kan wani ba, saboda ba ki gane
da lokacin da Allah zai ziyarce ki ba.”

*Yesu a haikali*
*(Mattiyu 21.12-17; Markus 11.15-19; Yohanna 2.13-22)*

45 Sai ya shiga filin haikali, ya fara korar masu sayar da kaya. 46 Ya ce musu, “A
rubuce, yake cewa, ‘Gidana, zai zama gidan addu’a,’* amma ga shi kun mai da shi
‘kogon ’yan fashi.’ ”†
47 Kowace rana, ya yi ta koyarwa a haikalin. Amma manyan firistoci, da malaman
dokoki, da shugabannin mutane, suna ƙoƙarin kashe shi. 48 Amma ba su sami hanyar
yin haka ba, domin kalmominsa sun kama hankalin dukan mutanen.

# 20

*An yi shakkar ikon Yesu*
*(Mattiyu 21.23-27; Markus 11.27-33)*

1 Wata rana da Yesu yana koyar da mutane, yana musu wa’azin bishara a filin
haikalin, sai manyan firistoci da malaman dokoki, tare da dattawan suka zo wurinsa.
2 Suka ce masa, “Gaya mana, da wane iko kake yin waɗannan abubuwa. Wa ya ba
ka wannan ikon?”
3 Ya amsa ya ce, “Ni ma zan yi muku wata tambaya. Ku faɗa mini, 4 baftismar
Yohanna, daga sama ne ta fito, ko kuwa daga wurin mutane ne?”
5 Sai suka yi shawara da junansu, suka ce, “In muka ce, ‘Daga sama ne,’ zai tambaya,
‘To, don me ba ku gaskata shi ba?’ 6 Amma in kuma muka ce, ‘Daga mutane ne,’ dukan
mutanen za su jajjefe mu da duwatsu, domin sun tabbata cewa, Yohanna annabi ne.”
7 Don haka, sai suka amsa cewa, “Ba mu san inda ta fito ba.”
8 Yesu ya ce, “To, ni ma ba zan gaya muku, ko da wane iko ne, nake yin waɗannan
abubuwa ba.”

*Misalin ’yan haya*
*(Mattiyu 21.33-46; Markus 12.1-12)*

9 Sai ya ci gaba da gaya wa mutanen wannan misali ya ce, “Wani mutum ya yi gonar
inabi, sai ya ba da hayarta ga waɗansu manoma, sa’an nan ya yi wata doguwar tafiya.
10 A lokacin girbi, sai ya aiki bawa zuwa wurin masu hayan, don su ba shi daga cikin
’ya’yan inabin. Amma ’yan hayan suka yi wa bawan nan dūka, suka kore shi hannu
wofi. 11 Ya sāke aikan wani bawa, shi ma suka yi masa dūka, suka kunyata shi, suka
kuma kore shi hannu wofi. 12 Har yanzu, ya sāke aikan na uku, amma suka ji masa
rauni, suka jefar da shi waje.
13 “Sai mai gonar inabin ya ce, ‘Me zan yi? Zan aiki ɗana da nake ƙauna, wataƙila
za su girmama shi.’
14 “Amma da ’yan hayan suka gan shi, sai suka tattauna zancen, suka ce, ‘Wannan
shi ne magājin, mu kashe shi sa’an nan gādon zai zama namu!’ 15 Sai suka fitar da
shi waje, suka kashe shi.
“To, me mai gonar inabin zai yi da su? 16 Zai zo ya karkashe masu hayan nan, ya
ba wa waɗansu gonar inabin.”
Da mutanen suka ji wannan, sai suka ce, “Allah ya sawwaƙa!”
17 Yesu ya zura musu ido ya ce, “To, mene ne ma’anar abin da aka rubuta cewa,
“ ‘Dutsen da magina suka ƙi,
shi ne kuwa ya zama dutsen kan ginin’*,†

* 19:46 Ish 56.7 † 19:46 Irm 7.11 * 20:17 Ko kuwa dutsen kusurwa † 20:17 Zab 118.22

18 Duk wanda ya fāɗi a kan dutsen nan, zai kakkarye. Kuma in dutsen nan ya fāɗi a
kan wani, zai murƙushe shi."
19 Malaman dokoki da manyan firistoci, suka nemi hanyar kama shi nan da nan,
domin sun san cewa, ya yi wannan misali a kansu ne, amma suna jin tsoron mutane.

*Biyan haraji ga Kaisar*
*(Mattiyu 22.15-22; Markus 12.13-17)*

20 Sai suka sa masa ido, suka aiki 'yan leƙen asiri, waɗanda suka nuna kamar su
masu gaskiya ne, suna nufin su kama shi game da abin da zai faɗa, domin su ba da
shi ga gwamna mai mulki, da mai iko. 21 Sai 'yan leƙen asirin suka tambaye shi, suka
ce, "Malam, mun sani kana faɗin, kuma kana koyar da abin da yake daidai, ba ka
kuma nuna bambanci, amma kana koyar da hanyar Allah bisa ga gaskiya. 22 Daidai
ne mu biya haraji ga Kaisar, ko babu?"
23 Ya gane makircinsu, sai ya ce musu, 24 "Nuna mini dinari. Hoton wane ne, kuma
rubutun wane ne a kai?"
Suka amsa, "Na Kaisar."
25 Sai ya ce musu, "Ku ba wa Kaisar abin da yake na Kaisar, ku kuma ba wa Allah
abin da yake na Allah."
26 Ba su iya kama shi a kan abin da ya faɗa a fili ba. Amsarsa ya ba su mamaki,
shi ya sa suka yi shiru.

*Ba aure a tashin matattu*
*(Mattiyu 22.23-33; Markus 12.18-27)*

27 Waɗansu Sadukiyawa da suke cewa, ba tashin matattu, suka zo wurin Yesu da
tambaya cewa, 28 "Malam, Musa ya rubuta mana cewa, 'In ɗan'uwan wani mutum
ya mutu, ya bar mata amma ba 'ya'ya, dole mutumin ya aure gwauruwar, ya samo
wa ɗan'uwansa 'ya'ya.' 29 To, an yi waɗansu 'yan'uwa bakwai. Na fari ya auri wata
mace, ya mutu ba 'ya'ya. 30 Na biyun, 31 da na ukun suka aure ta. Haka nan dukansu
bakwai suka mutu babu 'ya'ya. 32 A ƙarshe, ita macen ma ta mutu. 33 Shin, a tashin
matattu, matar wa za tă zama? Tun da su bakwan nan, sun aure ta."
34 Yesu ya amsa ya ce, "Mutanen zamanin nan suna aure, suna kuma ba da aure,
35 amma su waɗanda aka ga sun cancantar kasancewa a zamanin can, da kuma
na tashin matattu, ba za su yi aure, ko su ba da aure ba. 36 Kuma ba za su sāke
mutuwa ba, gama su kamar mala'iku ne. Su 'ya'yan Allah ne, tun da su 'ya'yan
tashin matattu ne. 37 Amma bisa ga labari na bishiya nan, mai cin wuta da Musa ya
gani a jeji, ko Musa ma, ya nuna cewa, matattu suna tashi. Gama ya kira Ubangiji,
'Allah na Ibrahim, da Allah na Ishaku, da kuma Allah na Yaƙub.' 38 Shi ba Allah na
matattu ba ne, amma na masu rai ne, gama a gare shi, duka na da rai."
39 Sai waɗansu malaman dokoki suka amsa suka ce, "Ka faɗi daidai, malam!"
40 Kuma ba wanda ya sami ƙarfin halin yin masa waɗansu tambayoyi.

*Kiristi ɗan wane ne?*
*(Mattiyu 22.41-46; Markus 12.35-37)*

41 Sai Yesu ya ce musu, "Yaya suke cewa, 'Kiristi ɗan Dawuda ne?' 42 Dawuda da
kansa ya faɗa a cikin Zabura,
" 'Ubangiji ya ce wa Ubangijina,
"Zauna a hannun damana,
43 sai na sa abokan gābanka
su zama matashin sawunka." '‡
44 Dawuda ya kira shi 'Ubangiji.' Ta, yaya zai zama ɗansa?"
*(Mattiyu 23.1-36; Markus 12.38-40; Luka 11.37-54)*

‡ **20:43** Zab 110.1

[45] Yayinda dukan mutane suna cikin sauraronsa, sai Yesu ya ce wa almajiransa,
[46] “Ku yi hankali da malaman dokoki. Sukan so sa manyan riguna suna zaga, suna
sha’awan karɓan gaisuwa a wuraren kasuwanci, da kuma wuraren zama mafi daraja
a majami’u, da wuraren bangirma a bukukkuwa. [47] Suna mamaye gidajen gwauraye,
kuma don burga, suna dogayen addu’o’i. Ga irin waɗannan mutane, za a yi musu
hukunci mai tsanani sosai.”

# 21

### *Bayarwar gwauruwa*
### *(Markus 12.41-44)*

[1] Da Yesu ya ɗaga ido, sai ya ga waɗansu masu arziki suna sa baikonsu a ma’ajin
haikalin. [2] Ya kuma ga wata gwauruwa matalauciya, ta saka anini biyu. [3] Sai ya
ce, “Gaskiya ina faɗa muku, wacce nan gwauruwa matalauciya ta sa fiye da dukan
sauran. [4] Dukan mutanen nan sun ba da baikonsu daga cikin arzikinsu ne, amma ita
daga cikin talaucinta, ta saka duk abin da take da shi na rayuwa.”

### *Alamun ƙarshen zamani*
### *(Mattiyu 24.1,2; Markus 13.1,2)*

[5] Waɗansu daga cikin almajiransa, suka fara magana a kan yadda aka yi wa
haikalin ado da duwatsu masu kyau, da kuma kyautai da aka keɓe wa Allah. Amma
Yesu ya ce, [6] “Wannan abin da kuke kallo a nan, lokaci yana zuwa da ba za a bar
wani dutse a kan wani dutse ba. Kowannensu, za a rushe shi.”

### *(Mattiyu 24.3-14; Markus 13.3-13)*

[7] Suka tambaye shi suka ce, “Malam, yaushe waɗannan za su faru? Kuma wace
alama za tă nuna cewa suna dab da faruwa?”
[8] Ya amsa ya ce, “Ku lura, kada ku kuma a ruɗe ku. Gama da yawa za su zo a
cikin sunana, suna cewa, ‘Ai, ni ne shi,’ da kuma, ‘Lokaci ya yi kusa.’ Kada ku bi su.
[9] Sa’ad da kuka ji labarin yaƙe-yaƙe, da juye juyen mulki, kada ku tsorota. Dole ne
waɗannan abubuwa su fara faruwa, amma ƙarshen ba zai zo nan da nan ba.”
[10] Sai ya ce musu, “Al’umma za tă tasar wa al’umma, mulki zai tasar wa mulki.
[11] Za a yi manyan girgizar ƙasa, da yunwa, da annoba a wurare dabam-dabam, da
kuma abubuwa masu bantsoro, da manyan alamu daga sama.
[12] “Amma kafin duk abubuwa nan, za a kama ku a tsananta muku. Za a kai ku
majami’u, da kurkuku. Za a kuma kai ku gaban sarakuna da gwamnoni, kuma dukan
waɗannan saboda sunana. [13] Wannan zai sa ku zama shaidu a gare su. [14] Amma ku
yi ƙuduri, wato, ku shirya zuciyarku, a kan ba za ku damu ba kafin lokacin, game
da yadda za ku kāre kanku. [15] Gama zan ba ku kalmomi, da hikima waɗanda ba ko
ɗaya daga cikin maƙiyanku, za su iya tsayayya da ku, ko su ƙaryata. [16] Har iyayenku,
da ’yan’uwanku maza, da danginku, da abokanku ma, duk za su bashe ku, su kuma
kashe waɗansunku. [17] Duk mutane za su ƙi ku saboda ni. [18] Amma ko gashi ɗaya na
kanku, ba zai hallaka ba. [19] Ta wurin tsayawa da ƙarfi, za ku sami rai.

### *(Mattiyu 24.15-21; Markus 13.14-19)*

[20] “In kuka ga mayaƙa sun kewaye Urushalima, za ku sani rushewarta ya yi kusa.
[21] A lokacin nan, bari waɗanda suke Yahudiya, su gudu zuwa cikin duwatsu. Bari
waɗanda suke cikin birnin kuma su fita, bari kuma waɗanda suke ƙauye kada su
shiga birnin. [22] Gama wannan shi ne lokacin hukunci, saboda a cika duk abin da
aka rubuta. [23] Zai zama abin kaito ga mata masu ciki, da mata masu renon ’ya’ya, a
waɗancan kwanakin! Za a yi baƙin ciki mai tsanani a ƙasar, da kuma fushi mai
tsanani a kan mutanen nan. [24] Za a kashe su da takobi, a kuma ɗauke su ’yan

kurkuku, zuwa dukan al'ummai. Al'ummai za su tattaka Urushalima, har sai lokacin
Al'ummai ya cika.

*(Mattiyu 24.29-31; Markus 13.24-27)*

25 “Za a yi alamu a cikin rana, da cikin wata, da cikin taurari. A duniya, al'ummai
za su yi baƙin ciki, su kuma rikice don tsoro, saboda ruri da kuma tafasar teku.
26 Mutane za su suma don tsoro, za su kuma yi fargaba, a kan abin da yake zuwa a
bisan duniya, gama za a girgiza duniyar taurarin sararin sama. 27 A lokacin ne za
su ga Ɗan Mutum yana zuwa cikin girgije, da iko, da ɗaukaka mai girma. 28 Sa'ad
da waɗannan abubuwa sun fara faruwa, ku tashi tsaye, ku ɗaga kawunanku, domin
fansarku yana matsowa kusa.”

*(Mattiyu 24.32-35; Markus 13.28-31)*

29 Sai ya gaya musu wannan misali ya ce, “Ku dubi itacen ɓaure da dukan itatuwa.
30 A duk lokacin da sun fara fitar da ganye, za ku gani da kanku, ku san cewa, damina
ta yi kusa. 31 Haka ma, in kuka ga waɗannan abubuwa suna faruwa, ku sani mulkin
Allah ya yi kusa.

32 “Gaskiya nake gaya muku, ba shakka, wannan zamani ba zai shuɗe ba, sai dukan
waɗannan abubuwa sun cika. 33 Sama da ƙasa za su shuɗe, amma kalmomina ba za
su taɓa shuɗewa ba.

34 “Ku lura fa don kada son jin daɗi na banza, da shaye-shaye, da damuwa na
rayuwa su rinjayi zuciyarku, har ranar ta auko muku ba tsammani kamar tarko.
35 Gama za tă zo a kan kowa da yake kan dukan duniya. 36 Ku yi tsaro kullum, ku yi
addu'a don ku iya kuɓuta daga dukan waɗannan abubuwa da suke kusan faruwa,
don ku iya tsayawa a gaban Ɗan Mutum.”

37 Kowace rana, Yesu yakan je haikalin ya yi koyarwa, da kowace yamma kuma,
ya je ya kwana a kan tudun da ake kira Dutsen Zaitun. 38 Da sassafe kuma, dukan
mutanen suka zo haikalin, don su saurare shi.

## 22

*Yahuda ya yarda ya bashe Yesu*

*(Mattiyu 26.1-5,14,16; Markus 14.1,2,10,11; Yohanna 11.45-53)*

1 Yanzu fa, Bikin Burodi Marar Yistin da ake kira Bikin Ketarewa ya yi kusa,
2 manyan firistoci da malaman dokoki kuma suna neman yadda za su kashe Yesu
a ɓoye, don suna tsoron mutane. 3 Shaiɗan kuwa ya shiga Yahuda, wanda ake kira
Iskariyot, ɗaya daga cikin Sha Biyun. 4 Sai Yahuda ya je ya tattauna da manyan
firistoci, da ma'aikatan 'yan gadin haikali, a kan yadda zai ba da Yesu a gare su.
5 Suka kuwa yi murna, suka yarda su ba shi kuɗi. 6 Ya ko yarda, ya fara neman
zarafin da zai ba da Yesu a gare su, sa'ad da taro ba sa nan tare da shi.

*Abincin yamma na ƙarshe*

*(Mattiyu 26.17-25; Markus 14.12-21; Yohanna 13.21-30)*

7 Sai ranar Bikin Burodi Marar Yisti ta kewayo, wato, ranar hadayar ɗan ragon
kafara na Bikin Ketarewa. 8 Sai Yesu ya aiki Bitrus da Yohanna, ya ce musu, “Ku je
ku yi shirye-shiryen Bikin Ketarewar da za mu ci.”

9 Suka tambaye shi suka ce, “Ina kake so mu je mu yi shirin?”

10 Ya amsa ya ce, “Sa'ad da kuka shiga cikin gari, za ku sadu da wani mutum yana
ɗauke da tulun ruwa. Ku bi shi zuwa gidan da zai shiga. 11 Ku ce wa maigidan,
Malam ya aike mu mu ce maka, ‘Ina ɗakin baƙi, inda ni da almajiraina za mu ci
abincin Bikin Ketarewa?’ 12 Zai nuna muku wani babban ɗakin sama a shirye. Nan
za ku yi shirin.”

13 Sai suka tafi, suka kuma iske kome kamar yadda Yesu ya faɗa musu. Sai suka
shirya Bikin Ketarewa.

*(Mattiyu 26.26-30; Markus 14.22-26; 1 Korintiyawa 11.23-25)*

14 Da lokaci ya yi, sai Yesu ya zauna tare da manzanninsa don cin abinci. 15 Sai ya
ce musu, “Na yi marmari ƙwarai don in ci wannan Bikin Ketarewa tare da ku, kafin
in sha wahala. 16 Ina dai gaya muku, ba zan ƙara cinsa ba, sai ya sami cika a mulkin
Allah.”
17 Bayan ya ɗauki kwaf ruwan inabi, ya yi godiya, sai ya ce, “Ku karɓa, ku rarraba
wa junanku. 18 Ina dai gaya muku, ba zan ƙara sha daga ’ya’yan inabi ba, sai mulkin
Allah ya zo.”
19 Sai ya ɗauki burodi ya yi godiya, ya kakkarya ya ba su, da cewa, “Wannan jikina
ne, da aka bayar dominku. Ku riƙa yin haka don tunawa da ni.”
20 Haka kuma, bayan abincin, ya ɗauki kwaf ruwan inabi ya ce, “Wannan kwaf
ruwan inabi shi ne, na sabon alkawari cikin jinina, da aka zubar dominku. 21 Amma
hannun wanda zai ci amanata, yana cin abincin tare da ni. 22 Ɗan Mutum zai mutu
kamar yadda aka ƙaddara, amma kaiton mutumin da zai bashe shi.” 23 Sai suka fara
tambayar junansu, ko wane ne a cikinsu zai yi wannan.
24 Gardama ta tashi a tsakaninsu, a kan ko wane ne a cikinsu ya fi girma. 25 Yesu
ya ce musu, “Sarakunan Al’ummai suna nuna iko a kan mutanensu, kuma waɗanda
suke nuna iko a kansu, suna kiran kansu Masu Taimakon mutane. 26 Amma ku, kada
ku zama haka. A maimakon haka, sai dai wanda ya fi girma a cikinku, ya zama
kamar wanda ya fi ƙanƙanta, wanda kuma ke mulki, ya zama kamar mai hidima.
27 Wane ne ya fi girma? Wanda yake zaune a tebur ne, ko kuma shi da yake yin
hidima? Ashe, ba wanda yake zaune a tebur ba ne? Amma ga ni, ni mai yin hidima
ne a cikinku. 28 Ku ne kuka tsaya tare da ni a gwaje-gwajen da na sha. 29 Daidai
kamar yadda Ubana ya ba ni mulki, haka ni ma nake ba ku. 30 Saboda ku ci, ku sha
a teburina a cikin mulkina. Kuma ku zauna a kan gadon sarauta, ku yi wa kabilu
goma sha biyu na Isra’ila shari’a.

*(Mattiyu 26.31-35; Markus 14.27-31; Yohanna 13.36-38)*

31 “Siman, Siman, Shaiɗan ya nemi izini ya sheƙe ka*kamar alkama. 32 Amma na yi
maka addu’a, Siman, domin kada bangaskiyarka ta kāsa. Bayan ka juyo, ka ƙarfafa
’yan’uwanka.”
33 Amma ya amsa ya ce, “Ubangiji, ina a shirye in tafi tare da kai har kurkuku, ko
mutuwa ma.”
34 Yesu ya ce, “Ina gaya maka Bitrus, kafin zakara ya yi cara yau, za ka yi mūsun
sanina sau uku.”
35 Sai Yesu ya tambaye, su ya ce, “Lokacin da na aike ku ba tare da jakar kuɗi, ko
jaka, ko takalma ba, kun rasa wani abu?”
Suka amsa, “Babu.”
36 Ya ce musu, “Amma yanzu, in kuna da jakar kuɗi, ko jaka, ku ɗauka. In kuma
ba ku da takobi, ku sayar da rigarku, ku saya. 37 A rubuce yake cewa, ‘An lissafta shi
tare da masu zunubi.’ Ina kuwa gaya muku, dole wannan ya cika a kaina. I, abin da
aka rubuta a kaina yana kusan cikawa.”
38 Almajiran suka ce, “Duba Ubangiji, ga takuba biyu.”
Yesu ya ce, “Ya isa.”

### *Yesu ya yi addu’a a Dutsen Zaitun*
*(Mattiyu 26.36-46; Markus 14.32-42)*

39 Yesu ya fita zuwa Dutsen Zaitun kamar yadda ya saba, almajiransa kuma suka
bi shi. 40 Da ya kai wurin, sai ya ce musu, “Ku yi addu’a don kada ku fāɗi cikin

* **22:31** Girik yana da ku ne a nan

jarraba.” 41 Sai ya janye daga wurinsu, misalin nisan jifa, ya durƙusa a ƙasa ya yi
addu’a, 42 “Uba, in ka yarda, ka ɗauke mini wannan kwaf, amma ba nufina ba, sai
dai naka.” 43 Wani mala’ika daga sama ya bayyana gare shi, ya ƙarfafa shi. 44 Domin
tsananin azaba, sai ya ƙara himma cikin addu’a, zuffansa kuma na ɗigowa ƙasa
kamar jini.
45 Da ya tashi daga addu’a, ya koma inda almajiransa suke, sai ya iske su suna
barci, daga gajiyar baƙin ciki. 46 Ya tambaye su, “Don me kuke barci? Ku tashi ku yi
addu’a, don kada ku fāɗi cikin jarraba.”

*An kama Yesu*
*(Mattiyu 26.47-56; Markus 14.43-50; Yohanna 18.3-11)*

47 Yana cikin magana sai ga taro sun zo. Mutumin nan da ake kira Yahuda, ɗaya
daga cikin Sha Biyun, shi ya bi da su. Sai ya matso kusa da Yesu don yǎ yi masa
sumba. 48 Amma Yesu ya tambaye shi ya ce, “Yahuda, ashe, da sumba za ka bashe
Ɗan Mutum?”
49 Da masu bin Yesu suka ga abin da zai faru, sai suka ce, “Ubangiji, mu yi sara da
takubanmu ne?” 50 Sai ɗayansu ya kai sara ga bawan babban firist, ya sare kunnen
damansa.
51 Amma Yesu ya amsa ya ce, “Kada a ƙara yin wannan!” Sai ya taɓa kunnen
mutumin da aka sara, ya warkar da shi.
52 Sai Yesu ya ce wa manyan firistoci, da ma’aikatan ’yan gadin haikali, da dattawa,
waɗanda suka zo don su kama shi, “Ina jagoran wani tawaye ne, da za ku zo da
takuba da sanduna? 53 Kullum ina tare da ku a filin haikali, amma ba ku kama ni ba.
Amma wannan ne sa’a naku, lokacin da duhu yake mulki.”

*Bitrus ya yi mūsun sanin Yesu*
*(Mattiyu 26.57,58,67-75; Markus 14.53,54,66-72; Yohanna 18.12-18,25-27)*

54 Sai suka kama shi suka kai shi gidan babban firist. Bitrus ya bi su daga nesa.
55 Amma da suka hura wuta a tsakiyar harabar gidan, kowa ya zauna, sai Bitrus ya
zo ya zauna tare da su. 56 Wata baiwa ta gan shi zaune kusa da wutar. Ta dube shi
sosai sa’an nan, ta ce, “Ai, wannan mutum ma yana tare da shi.”
57 Amma ya yi mūsu ya ce, “Mace, ban san shi ba!”
58 Bayan ɗan lokaci kaɗan, wani dabam ya gan shi ya ce, “Kai ma ɗayansu ne.”
Bitrus ya amsa ya ce, “Kai, ba na cikinsu!”
59 Bayan kamar sa’a ɗaya, sai wani mutum ya ce, “Ba shakka, mutumin nan ma
yana tare da shi, don shi mutumin Galili ne.”
60 Bitrus ya amsa ya ce, “Kai, ban ma san abin da kake magana a kai ba!” Yana
cikin magana, sai zakara ya yi cara. 61 Ubangiji kuma ya juya ya kafa wa Bitrus ido.
Sai Bitrus ya tuna da maganar da Ubangiji ya ce masa, “Kafin zakara ya yi cara yau,
za ka yi mūsun sanina sau uku.” 62 Sai ya fita waje, ya yi kuka mai zafi.

*Masu gadi sun yi wa Yesu ba’a*
*(Mattiyu 26.59-66; Markus 14.55-64; Yohanna 18.19-24)*

63 Mutanen da suke gadin Yesu suka fara masa ba’a da dūka. 64 Suka rufe masa
idanu suna tambaya cewa, “Ka yi annabci! Wa ya mare ka?” 65 Suka kuma yi masa
waɗansu baƙaƙen maganganu masu yawa.

*Yesu a gaban Bilatus da Hiridus*

66 Da gari ya waye, sai majalisar dattawa na mutane, da manyan firistoci, da
malaman dokoki, suka taru wuri ɗaya. Sai aka kawo Yesu a gabansu. 67 Suka ce,
“Ka faɗa mana, ko kai ne Kiristi?”

Yesu ya amsa ya ce, “Ko na gaya muku, ba za ku gaskata ni ba, 68 in kuma na yi
muku tambaya ba za ku iya ba ni amsa ba. 69 Amma daga yanzu, Ɗan Mutum zai
zauna a hannun dama na Allah Mai Iko.”
70 Sai dukansu suka yi tambaya suka ce, “Wato, kai Ɗan Allah ke nan?”
Ya amsa ya ce, “Kun faɗa daidai, ni ne.”
71 Sai suka ce, “Wace shaida kuma muke nema? Ai, mun ji abin da ya ce da bakinsa.”

# 23

*(Mattiyu 27.1,2,11-14; Markus 15.1-5; Yohanna 18.28-38)*

1 Sai dukan majalisa suka tashi, suka kai shi gaban Bilatus. 2 Suka fara zarginsa
suna cewa, “Mun sami wannan mutum yana rikitar da al’ummarmu. Yana hana a
biya haraji ga Kaisar. Yana kuma cewa, shi Kiristi ne, sarki kuma.”
3 Sai Bilatus ya tambayi Yesu ya ce, “Kai ne sarkin Yahudawa?”
Yesu ya amsa ya ce, “I, haka yake, kamar yadda ka faɗa.”
4 Sai Bilatus ya sanar wa manyan firistoci da taron ya ce, “Ni fa, ban sami wani
ainihin abin zargi game wannan mutum nan ba.”
5 Amma suka nace, suna cewa, “Yana tā da hankulan mutane, ko’ina a Yahudiya
da koyarwarsa. Ya fara daga Galili, ga shi har ya kai nan.”
6 Da Bilatus ya ji haka, sai ya yi tambaya, “Ko shi mutumin Galili ne?” 7 Da ya ji
cewa, Yesu yana ƙarƙashin mulkin Hiridus ne, sai ya aika da shi zuwa wurin Hiridus,
don a lokacin Hiridus yana Urushalima.
8 Da Hiridus ya ga Yesu, sai ya yi murna ƙwarai, don tun dā ma yana marmari ya
gan shi a kan abin da ya ji game da shi. Ya yi fata ya ga Yesu, yǎ kuma yi waɗansu
ayyukan banmamaki. 9 Ya yi masa tambayoyi masu yawa, amma Yesu bai ba shi
ko amsa ba. 10 Manyan firistoci da malaman dokoki suna tsaye a wurin, suna kawo
zargi masu ƙarfi a kansa. 11 Sai Hiridus da sojojinsa suka wulaƙanta shi, suka yi
masa ba’a. Sa’an nan, suka sa masa babban riga, suka mai da shi wurin Bilatus. 12 A
ranar, Hiridus da Bilatus suka zama abokan juna, don tun dā ma, su abokan gāba ne.

*(Mattiyu 27.15-26; Markus 15.6-15; Yohanna 18.39–19.16)*

13 Bilatus ya tara manyan firistoci, da masu mulki, da mutane, 14 ya ce musu, “Kun
kawo mini wannan mutum, a matsayin wanda yana zuga mutane su yi tawaye. Na
bincike shi a gabanku, ban ga a kan me kuka kawo kararsa ba. 15 Haka ma Hiridus,
shi ya sa ya dawo da shi nan wurinmu. Kamar yadda ku ma kun gani, ba abin da
mutumin nan ya yi, da ya isa mutuwa. 16 Saboda haka, zan yi masa bulala, in sāke
shi.”*
18 Suka yi ihu gaba ɗaya suka ce, “A yi gaba da wannan mutum! A sake mana
Barabbas!” 19 (Barabbas yana kurkuku saboda laifin tā da hankali a birnin, da kuma
don kisankai.)
20 Sai Bilatus ya sāke yin musu magana don yana so ya saki Yesu. 21 Amma sai suka
ci gaba da ihu, suna cewa, “A gicciye shi! A gicciye shi!”
22 Ya sāke ce musu, sau na uku, “Don me? Wane laifi wannan mutum ya yi? Ni dai
ban same shi da wani dalilin da ya isa a kashe shi ba. Saboda haka, zan sa a hore
shi, sa’an nan in sāke shi.”
23 Amma suna ihu, suna nacewa, suna cewa, dole a gicciye shi, har ihunsu ya rinjaye
shi. 24 Sai Bilatus ya biya bukatarsu da ya ji roƙonsu. 25 Ya saki mutumin da aka jefa
a kurkuku saboda tā da hankali, da kisankai, shi wanda suka roƙa. Sa’an nan ya ba
da Yesu ga nufinsu.

---

* **23:16** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da 17 A lokacin idi kuwa lalle ne ya sakar musu ɗaurarre guda.

### *Gicciyewa*
### *(Mattiyu 27.31-44; Markus 15.21-32; Yohanna 19.17-27)*

26 Sa'ad da suna tafiya da Yesu, sai wani da ake kira Siman, mutumin Sairin, yana
zuwa daga ƙauye. Suka kama shi, suka aza masa gicciyen, suka tilasta shi ya ɗauki
gicciyen, ya bi Yesu a baya. 27 Mutane da yawa sosai suka bi shi, a cikinsu ma da
mata waɗanda suka yi makoki da kuka dominsa. 28 Yesu ya juya, ya ce musu, "'Yan
matan Urushalima, kada ku yi kuka saboda ni, amma ku yi kuka saboda kanku, da
kuma saboda 'ya'yanku. 29 Gama lokaci yana zuwa da za ku ce, 'Masu albarka ne
bakararru, wato, mata marasa haihuwa, da mahaihuwar da ba su taɓa haihuwa ba,
da kuma mama da ba su taɓa shayar da nono ba!' 30 Sa'an nan

" 'za su ce wa duwatsu,
"Ku fāɗi a kanmu!"
Za su ce wa tuddai kuma,
"Ku rufe mu!" '†

31 Gama in mutane suna yin waɗannan abubuwa a lokacin da itace na ɗanye, me zai
faru in ya bushe?"

32 Tare da shi akwai mutum biyu masu laifi, da aka tafi da su don a gicciye. 33 Da
suka isa wurin da ake kira "Koƙon Kai," nan suka gicciye shi, tare da masu laifin
nan, ɗaya a hannun damansa, ɗayan kuma a hagunsa. 34 Yesu ya ce, "Ya Uba ka yi
musu gafara, don ba su san abin da suke yi ba." Suka rarraba tufafinsa ta wurin jefa
ƙuri'a.

35 Mutanen suka tsaya suna kallo. Har masu mulki ma suka yi masa ba'a, suna
cewa, "Ya ceci waɗansu, to, ya ceci kansa in shi ne Kiristi na Allah, Zaɓaɓɓe."

36 Sojoji su ma, suka zo suka yi masa ba'a. Suka miƙa masa ruwan tsami. 37 Suka
ce, "In kai ne sarkin Yahudawa, ka ceci kanka mana."

38 Bisa da shi kuma akwai rubutun da ya ce,

WANNAN SHI NE SARKIN YAHUDAWA.

39 Ɗaya daga cikin masu laifin da aka gicciye a wurin ya zazzage shi ya ce, "Shin,
ba kai ne Kiristi ba? To, ka ceci kanka, ka kuma cece mu mana!"

40 Amma ɗayan mai laifi ya kwaɓe shi ya ce, "Ba ka da tsoron Allah ne, wai
saboda kana ƙarƙashin hukunci ɗaya tare da shi? 41 Horonmu, daidai aka yi mana,
sakamakon abin da muka yi ne. Amma wannan mutum, bai yi wani laifi ba."

42 Sai ya ce, "Yesu, ka tuna da ni sa'ad da ka shiga mulkinka."

43 Yesu ya amsa, ya ce masa, "Gaskiya nake faɗa maka, yau ɗin nan, za ka kasance
tare da ni, a mulkina a sama."

### *Mutuwar Yesu*
### *(Mattiyu 27.45-56; Markus 15.33-41; Yohanna 19.28-30)*

44 Yanzu kuwa wajen sa'a ta shida ne, kuma duhu ya rufe ko'ina a ƙasar, har zuwa
sa'a ta tara, 45 domin rana ta daina haskakawa. Labulen da yake cikin haikali kuma
ya yage kashi biyu. 46 Yesu ya yi kira da babbar murya ya ce, "Ya Uba, na danƙa
ruhuna a hannunka." Da ya faɗi haka, sai ya ja numfashi na ƙarshe.

47 Da jarumin ya ga abin da ya faru, sai ya yabi Allah ya ce, "Gaskiya, wannan
mutum mai adalci ne." 48 Da dukan mutanen da suka taru, domin shaidar waɗannan
abubuwa, suka ga abin da ya faru, sai suka buga ƙirjinsu suka tafi. 49 Amma dukan
mutanen da suka san Yesu, tare da mata da suka bi shi daga Galili, suka tsaya daga
nesa suna kallon abubuwan nan.

### *Binne Yesu*
### *(Mattiyu 27.57-61; Markus 15.42-47; Yohanna 19.38-42)*

50 Akwai wani mutum mai suna Yusuf, ɗan Majalisa, wanda shi nagari ne, mai
adalci, 51 shi dā ma bai yarda da shawararsu, da kuma abin da suka yi ba. Shi daga

† **23:30** Hos 10.8

Arimateya ne wani garin Yahudiya. Yana kuma jiran zuwa mulkin Allah. 52 Sai ya je
wurin Bilatus ya roƙa a ba shi jikin Yesu. 53 Sai ya saukar da jikin, ya nannaɗe shi a
cikin zanen lilin, ya sa shi a wani kabari da aka fafe a cikin dutse, wadda ba a taɓa
sa kowa ba. 54 An yi haka ne a Ranar Shirye-shirye, ranar Asabbaci kuma yana dab
da farawa.
55 Matan da suka zo tare da Yesu, daga Galili suka bi Yusuf suka ga kabarin, da
kuma yadda aka ajiye jikin. 56 Sa'an nan, suka koma gida, suka shirya kayan ƙanshi
da turare. Amma suka huta a ranar Asabbaci don kiyaye doka.

# 24

*Tashin Yesu daga matattu*
*(Mattiyu 28.1-10; Markus 16.1-8; Yohanna 20.1-10)*

1 Da sassafe a ranar farko ta mako, matan suka je kabarin, da kayan ƙanshin da
suka shirya. 2 Suka iske an riga an gungurar da dutsen daga bakin kabarin. 3 Amma
da suka shiga ciki, ba su iske jikin Ubangiji Yesu ba. 4 Yayinda suna cikin tunani a kan
wannan, nan take, ga waɗansu mutum biyu tsaye kusa da su, sanye da kaya masu
ƙyalli, kamar walƙiya. 5 A cikin tsoro, matan suka fāɗi da fuskokinsu a ƙasa, amma
mutanen suka ce musu, "Me ya sa kuke neman mai rai a cikin matattu? 6 Ba ya nan,
ya tashi! Ku tuna yadda ya gaya muku tun yana tare da ku a Galili cewa, 7 'Dole a
ba da Ɗan Mutum ga hannun masu zunubi, a kuma gicciye shi, a rana ta uku kuma
a tashe shi.' " 8 Sai suka tuna da maganarsa.
9 Da suka dawo daga kabarin, sai suka faɗa wa Sha Ɗayan nan da sauransu, dukan
waɗannan abubuwa. 10 Matan da suka gaya wa manzannin waɗannan abubuwa
su ne, Maryamu Magdalin, da Yowanna, da Maryamu uwar Yaƙub, da waɗansu da
suke tare da su. 11 Amma ba su gaskata matan ba, domin sun ɗauki kalmominsu
wani zancen banza ne. 12 Duk da haka, Bitrus ya tashi a guje zuwa kabarin. Da ya
sunkuya, sai ya ga ƙyallayen lilin kaɗai a kwance. Sai ya koma yana tunani a ransa,
a kan abin da ya faru.

*A hanyar Emmawus*
*(Markus 16.12,13)*

13 A wannan rana kuma, biyu daga cikinsu suna tafiya zuwa wani ƙauye, da ake
kira Emmawus, da suke kusan mil bakwai daga Urushalima. 14 Suna magana da
juna a kan dukan abubuwan da suka faru. 15 Da suna magana, kuma suna tattauna
waɗannan abubuwa da junansu, sai Yesu da kansa ya zo yana tafiya tare da su.
16 Amma ba a ba su ikon gane shi ba.
17 Sai ya tambaye, su ya ce, "Mene ne kuke tattaunawa da juna a cikin tafiyarku?"
Suka tsaya shiru, da damuwa a fuskarsu. 18 Ɗaya daga cikinsu, mai suna Kiliyobas,
ya tambaye shi ya ce, "Ashe, kai baƙo ne a Urushalima, da ba ka san abubuwan da
suka faru a can, a cikin kwanakin nan ba?"
19 Sai ya yi tambaya, "Waɗanne abubuwa?"
Suka amsa suka ce, "Game da Yesu Banazare. Shi annabi ne, mai iko ne kuma cikin
ayyukansa da maganarsa, a gaban Allah da kuma dukan mutane. 20 Manyan firistoci
da masu mulkinmu sun ba da shi a yi masa hukuncin mutuwa, suka kuwa gicciye
shi. 21 Amma da, muna sa zuciya cewa, shi ne wanda zai fanshi Isra'ila. Bugu da ƙari
kuma yau kwana uku ke nan tun da wannan abin ya faru. 22 Har wa yau, waɗansu
daga cikin matanmu sun ba mu mamaki. Sun je kabarin da sassafen nan, 23 amma
ba su sami jikinsa ba. Sun dawo sun faɗa mana cewa, sun ga wahayi na mala'iku, da
suka ce yana da rai. 24 Sa'an nan, waɗansu abokanmu suka je kabarin, suka kuma
tarar da kome kamar yadda matan suka faɗa, amma shi, ba su gan shi ba."

25 Sai ya ce musu, “Ashe, ku marasa azanci ne, masu nauyin zuciyar gaskata, da
dukan abin da annabawa suka faɗa! 26 Ai, dole Kiristi yă sha waɗannan wahalolin,
kafin yă shiga ɗaukakarsa. 27 Sai ya fara bayyana musu daga Musa da dukan
Annabawa, abin da dukan Nassi ya faɗa a kansa.”
28 Da suka yi kusa da ƙauyen da za su, sai Yesu ya yi kamar zai ci gaba. 29 Amma
suka matsa masa suka ce, “Sauka wurinmu, don dare ya kusa, rana ta kusa fāɗuwa.”
Sai ya sauka wurinsu.
30 Da ya zauna a tebur tare da su, sai ya ɗauki burodi, ya yi godiya, ya kakkarya
ya fara ba su. 31 Sa’an nan idanunsu suka buɗe, suka gane shi. Sai ya ɓace musu.
32 Suka tambayi juna, “Ashe, shi ya sa zukatanmu suka kuna a cikinmu, sa’ad da yake
magana da mu a hanya, yana bayyana mana Nassi.”
33 Suka tashi nan da nan suka koma Urushalima. A can suka sami Sha Ɗayan nan
da waɗanda suke tare da su a wuri ɗaya, 34 suna cewa, “Gaskiya ne! Ubangiji ya
tashi, ya kuma bayyana ga Siman” 35 Sai su biyun nan suka ba da labarin abin da ya
faru a hanya, da kuma yadda suka gane Yesu yayinda ya kakkarya burodin.

### *Yesu ya bayyana ga almajirai*
*(Mattiyu 28.16-20; Markus 16.14-18; Yohanna 20.19-23; Ayyukan Manzanni 1.6-8)*

36 Suna cikin wannan zance, sai ga Yesu da kansa tsaye a tsakiyarsu. Sai ya ce
musu, “Salama a gare ku!”
37 Suka firgita, suka tsorota, suna tsammani fatalwa ce suka gani. 38 Sai ya ce musu,
“Don me kuke damuwa, kuke kuma shakka a zuciyarku? 39 Ku duba hannuwana da
ƙafafuna. Ai, ni ne da kaina! Ku taɓa ni ku ji, ai, fatalwa ba ta da nama da ƙashi,
yadda kuke gani nake da su.”
40 Da ya faɗi haka, sai ya nuna musu hannuwansa da ƙafafunsa. 41 Kuma har
yanzu, suna cikin rashin gaskatawa, saboda murna da mamaki, sai ya tambaye su,
“Kuna da abinci a nan?” 42 Suka ba shi ɗan gasasshen kifi, 43 ya karɓa ya ci a gabansu.
44 Ya ce musu, “Wannan shi ne abin da na gaya muku tun ina tare da ku cewa, dole
a cika kome da aka rubuta game da ni, a cikin Dokar Musa, da Annabawa, da kuma
Zabura.”
45 Sai ya wayar da tunaninsu don su fahimci Nassi. 46 Ya ce musu, “Wannan shi ne
abin da aka rubuta, cewa dole Kiristi yă sha wahala, a rana ta uku kuma yă tashi daga
matattu. 47 Kuma a cikin sunansa za a yi wa’azin tuba da gafarar zunubai, ga dukan
ƙasashe. Za a kuwa fara daga Urushalima. 48 Ku ne shaidun waɗannan abubuwa.
49 Zan aika muku da abin da Ubana ya yi alkawari. Amma ku dakata a birnin tukuna,
sai an rufe ku da iko daga sama.”

### *Tashi zuwa sama*
*(Markus 16.19,20; Ayyukan Manzanni 1.9-11)*

50 Bayan ya kai su waje kusa da Betani, sai ya ɗaga hannuwansa ya sa musu albarka.
51 Yana cikin sa musu albarka, sai ya rabu da su. Aka ɗauke shi zuwa cikin sama.
52 Sai suka yi masa sujada, suka koma Urushalima cike da murna sosai. 53 Sai suka ci
gaba da zama a cikin haikalin, suna yabon Allah.

# Yohanna

### *Kalman ya zama mutum*

1 Tun farar farawa akwai Kalma, Kalman kuwa yana nan tare da Allah, Kalman
kuwa Allah ne. 2 Yana nan tare da Allah tun farar farawa. 3 Ta wurin Kalman ne
aka halicci dukan abubuwa. In ba tare da shi ba, babu abin da aka yi wanda aka yi.
4 A cikinsa rai ya kasance, wannan rai kuwa shi ne hasken mutane. 5 Hasken yana
haskakawa cikin duhu, amma duhun bai rinjaye shi ba.

6 Akwai wani mutumin da aka aiko daga Allah; mai suna Yohanna. 7 Ya zo a
matsayin mai shaida domin yă ba da shaida game da wannan haske, don ta wurinsa
dukan mutane su ba da gaskiya. 8 Shi kansa ba shi ne hasken ba; sai dai ya zo a
matsayin shaida ne kaɗai ga hasken.

9 Haske na gaskiya da yake ba da haske ga kowane mutum mai shigowa duniya.*
10 Yana a duniya, kuma ko da yake an yi duniya ta wurinsa ne, duniya ba tă gane
shi ba. 11 Ya zo wurin abin da yake nasa, amma nasa ɗin ba su karɓe shi ba. 12 Duk
da haka dukan waɗanda suka karɓe shi, ga waɗanda suka gaskata a sunansa, ya ba
su iko su zama ’ya’yan Allah 13 ’ya’yan da aka haifa ba bisa hanyar ’yan adam,† ko
shawarar mutum ko nufin namiji ba, sai dai haifaffu bisa ga nufin Allah.

14 Kalman ya zama mutum, ya kuwa zauna a cikinmu. Muka ga ɗaukakarsa,
ɗaukaka ta wanda yake Ɗaya kuma Makaɗaici, wanda ya zo daga wurin Uba, cike
da alheri da gaskiya.

15 (Yohanna ya ba da shaida game da shi. Ya ɗaga murya yana cewa, “Wannan shi
ne wanda na ce, ‘Mai zuwa bayana ya fi ni girma domin yana nan kafin ni.’ ”) 16 Daga
yalwar alherinsa dukanmu muka sami albarka bisa albarka. 17 Gama an ba da doka
ta wurin Musa; alheri da gaskiya kuwa sun zo ne ta wurin Yesu Kiristi. 18 Ba wanda
ya taɓa ganin Allah, sai dai Allah da yake Ɗaya da kuma Makaɗaici wanda yake a
gefen Uba, shi ne ya bayyana shi.

### *Yohanna Mai Baftisma ya ce ba shi ne Kiristi ba*

19 To, ga shaidar Yohanna sa’ad da Yahudawan Urushalima suka aiki firistoci da
Lawiyawa su tambaye shi ko shi wane ne. 20 Bai yi mūsu ba, amma ya shaida a fili
cewa, “Ba ni ne Kiristi ba.”

21 Sai suka tambaye shi suka ce, “To, wane ne kai? Kai ne Iliya?”

Ya ce, “A’a, ni ba shi ba ne.”

“Kai ne Annabin nan?”

Ya amsa ya ce, “A’a.”

22 A ƙarshe suka ce, “Wane ne kai? Ka ba mu amsa don mu mayar wa waɗanda
suka aike mu. Me kake ce da kanka?”

23 Yohanna ya amsa da kalmomin annabi Ishaya, “Ni murya ne mai kira a hamada,
‘Ku miƙe hanya domin Ubangiji.’ ”‡

24 To, waɗansu Farisiyawan da aka aika 25 suka tambaye shi suka ce, “Don me kake
yin baftisma in kai ba Kiristi ba ne, ba kuwa Iliya ba, ba kuma annabin nan ba?”

26 Yohanna ya amsa ya ce, “Ni dai ina baftisma da ruwa ne, amma a cikinku akwai
wani tsaye da ba ku sani ba. 27 Shi ne mai zuwa bayana, wanda ko igiyar takalmansa
ma ban isa in kunce ba.”

28 Wannan duk ya faru ne a Betani a ƙetaren Urdun, inda Yohanna yake yin
baftisma.

---

* **1:9** Ko kuwa Wannan ne haske na gaskiya da yake ba da haske ga kowane mutumin da yake shigowa duniya
† **1:13** Girik na jini ‡ **1:23** Ish 40.3

*Yesu Ɗan Rago na Allah*

29 Kashegari Yohanna ya ga Yesu yana zuwa wajensa sai ya ce, “Ku ga, ga Ɗan Rago
na Allah mai ɗauke zunubin duniya! 30 Wannan shi ne wanda nake nufi sa’ad da na
ce, ‘Mutum mai zuwa bayana ya fi ni girma, domin yana nan kafin ni.’ 31 Ko ni ma
dā ban san shi ba, sai dai abin da ya sa na zo ina baftisma da ruwa shi ne domin a
bayyana shi ga Isra’ila.”
32 Sai Yohanna ya ba da wannan shaida, “Na ga Ruhu ya sauko kamar kurciya daga
sama ya zauna a kansa. 33 Dā ban san shi ba, sai dai wanda ya aiko ni in yi baftisma
da ruwa ya gaya mini cewa, ‘Mutumin da ka ga Ruhu ya sauko ya kuma zauna a
kansa shi ne wanda zai yi baftisma da Ruhu Mai Tsarki.’ 34 Na gani na kuma shaida
cewa wannan Ɗan Allah ne.”

*Almajiran Yesu na farko*

35 Kashegari kuma Yohanna yana can tare da biyu daga cikin almajiransa. 36 Da ya
ga Yesu yana wucewa, sai ya ce, “Ku ga, ga Ɗan Rago na Allah!”
37 Da almajiran nan biyu suka ji ya faɗi haka, sai suka bi Yesu. 38 Da juyewa, sai
Yesu ya ga suna bin sa, sai ya tambaye, su ya ce, “Me kuke nema?”
Suka ce, “Rabbi” (wato, “Malam”), “ina kake da zama?”
39 Ya amsa musu ya ce, “Ku zo, za ku kuma gani.”
Saboda haka suka je suka ga inda yake da zama, suka kuma zauna a can tare da
shi. Wajen sa’a ta goma ce kuwa.
40 Andarawus ɗan’uwan Siman Bitrus, yana ɗaya daga cikin biyun nan da suka bi
Yesu bayan da suka ji maganar Yohanna a kan Yesu. 41 Abu na fari da Andarawus
ya yi shi ne ya sami ɗan’uwansa Siman ya gaya masa cewa, “Mun sami Almasihu”
(wato, Kiristi). 42 Ya kuma kawo shi wurin Yesu.
Yesu ya dube shi ya ce, “Kai ne Siman ɗan Yohanna. Za a ce da kai Kefas” (in an
fassara, Bitrus ke nan§).

*Yesu ya kira Filibus da Natanayel*

43 Kashegari Yesu ya yanke shawara yǎ tafi Galili. Da ya sami Filibus sai ya ce masa,
“Bi ni.”
44 Filibus, kamar Andarawus da Bitrus shi ma daga garin Betsaida ne. 45 Filibus
ya sami Natanayel ya kuma gaya masa, “Mun sami wanda Musa ya rubuta game da
shi a cikin Doka, kuma wanda annabawa suka rubuta a kansa, Yesu Banazare, ɗan
Yusuf.”
46 Natanayel ya ce, “A Nazaret! Wani abin kirki zai iya fito daga can?”
Filibus ya ce, “Zo ka gani.”
47 Da Yesu ya ga Natanayel yana zuwa, sai ya yi magana game da shi cewa, “Ga
mutumin Isra’ila na gaske wanda ba shi da ha’inci.”
48 Natanayel ya yi tambaya ya ce, “A ina ka san ni?”
Yesu ya amsa ya ce, “Na gan ka yayinda kake a gindin itacen ɓaure, kafin Filibus
yǎ kira ka.”
49 Sai Natanayel ya ce, “Rabbi, kai Ɗan Allah ne. Kai ne Sarkin Isra’ila.”
50 Yesu ya ce, “Ka gaskata domin na ce maka na gan ka a gindin itacen ɓaure. Za
ka ga abubuwan da suka fi haka.” 51 Sai ya ƙara da cewa, “Gaskiya nake gaya muku,
za ku ga sama a buɗe, mala’ikun Allah kuma suna hawa suna kuma sauka a kan Ɗan
Mutum.”

# 2

*Yesu ya mai da ruwa ya zama ruwan inabi*

§ **1:42** Da Kefas (Arameyik) da kuma Bitrus (Girik) na nufin dutse.

1 A rana ta uku sai aka yi bikin aure a Kana ta Galili. Mahaifiyar Yesu kuwa tana
can, 2 aka gayyaci Yesu da almajiransa su ma a auren. 3 Da ruwan inabi ya ƙare, sai
mahaifiyar Yesu ta ce masa, “Ba su da sauran ruwan inabi.”
4 Yesu ya ce, “Mace, me ya sa kike haɗa ni a wannan? Lokacina bai yi ba tukuna.”
5 Sai mahaifiyarsa ta ce wa bayin, “Ku yi duk abin da ya faɗa.”
6 Nan kusa kuwa akwai tulunan ruwa shida na dutse a ajiye, irin da Yahudawa
suke amfani da su don tsarkakewa bisa ga al’ada, kowace kan ci gallon kusan ashirin
zuwa talatin.
7 Sai Yesu ya ce wa bayin, “Ku ciccika tulunan da ruwa.” Suka kuwa ciccika su fal.
8 Sa’an nan ya ce musu, “Yanzu ku ɗiba ku kai wa uban bikin.”
Suka yi haka. 9 Uban bikin kuwa ya ɗanɗana ruwan da aka juya ya zama ruwan
inabi. Bai san daga ina ya fito ba, ko da yake bayin da suka ɗiba ruwan sun sani. Sai
ya kira angon waje ɗaya 10 ya ce, “Kowa yakan kawo ruwan inabi mafi kyau da fari,
sa’an nan marar kyan bayan baƙin sun sha da yawa; amma ka ajiye ruwan inabi
mafi kyau sai yanzu.”
11 Wannan shi ne na fari cikin abubuwan banmamakin da Yesu ya yi a Kana ta
Galili. Ta haka ya bayyana ɗaukakarsa, almajiransa kuwa suka ba da gaskiya gare
shi.

*Yesu ya tsabtacce haikali*

12 Bayan wannan sai ya tafi Kafarnahum tare da mahaifiyarsa da ’yan’uwansa da
kuma almajiransa. A can suka zauna ’yan kwanaki.

*(Mattiyu 21.12,13; Markus 11.15-17; Luka 19.45,46)*

13 Da lokacin Bikin Ketarewa na Yahudawa ya yi kusa, sai Yesu ya haura zuwa
Urushalima. 14 A filin haikali ya sami mutane suna sayar da shanu, tumaki da
tattabaru, waɗansu kuma zaune a tebur suna canjin kuɗi. 15 Saboda haka ya tuƙa
bulala ta igiyoyi, ya kori duka daga filin haikali, har da tumaki da shanu; ya watsar
da kuɗin masu canjin, ya birkice teburansu. 16 Ga masu sayar da tattabaru kuwa ya
ce, “Ku kwashe waɗannan daga nan! Don me za ku mai da gidan Ubana kasuwa!”
17 Sai almajiransa suka tuna cewa a rubuce yake, “Himma saboda gidanka zai cinye
ni.”*
18 Sai Yahudawa suka tambaye shi, “Wace abar banmamaki za ka nuna mana ka
tabbatar mana ikonka na yin duk waɗannan?”
19 Yesu ya amsa musu ya ce, “Ku rushe wannan haikali, zan kuwa sāke tā da shi
cikin kwana uku.”
20 Yahudawa suka ce, “Sai fa da aka shekara arba’in da shida ana ginin haikalin
nan, kai kuwa a cikin kwana uku za ka tā da shi?” 21 Amma haikalin da ya yi magana
jikinsa ne. 22 Bayan da ya tashi daga matattu, sai almajiransa suka tuna da abin da
ya faɗa. Sa’an nan suka gaskata Nassi da kuma kalmomin da Yesu ya yi.
23 To, yayinda yake a Urushalima a Bikin Ketarewa, mutane da yawa suka ga
abubuwan banmamakin da yake aikata suka kuma gaskata da sunansa. 24 Sai dai
Yesu bai amince da su ba, don ya san dukan mutane. 25 Ba ya bukatar shaidar mutum
game da mutum, don yă san abin da yake cikin zuciyar mutum.

# 3

*Yesu ya koyar da Nikodimus*

1 Akwai wani Bafarisiye mai suna Nikodimus, wani ɗan majalisar Yahudawa. 2 Ya
zo wurin Yesu da dad dare ya ce, “Rabbi, mun sani kai malami ne daga Allah. Gama
ba wanda zai iya yin waɗannan abubuwan banmamaki da kake yi in Allah ba ya
tare da shi.”

* **2:17** Zab 69.9

3 Yesu ya amsa ya ce, “Gaskiya nake faɗa maka, ba wanda zai iya ganin mulkin
Allah sai an sāke haihuwarsa.”
4 Nikodimus ya yi tambaya ya ce, “Yaya za a haifi mutum sa’ad da ya tsufa?
Tabbatacce ba zai sāke koma sau na biyu a cikin mahaifiyarsa don a haife shi kuma
ba!”
5 Yesu ya amsa ya ce, “Gaskiya nake faɗa maka, ba wanda zai iya ganin mulkin
Allah sai an haife shi ta wurin ruwa da kuma Ruhu. 6 Jiki yakan haifi jiki, amma
Ruhu yana haifi ruhu. 7 Kada ka yi mamaki da na ce, ‘Dole ne a sāke haifarku.’ 8 Iska
takan hura zuwa inda take so. Kai kakan ji motsinta, sai dai ba ka iya sanin inda take
fitowa ko kuwa inda za ta. Haka yake ga duk wanda aka haifa ta wurin Ruhu.”
9 Nikodimus ya yi tambaya ya ce, “Yaya wannan zai yiwu?”
10 Yesu ya ce, “Kai ma da kake malami na Isra’ila, ba ka fahimci waɗannan
abubuwa ba? 11 Gaskiya nake faɗa maka, muna magana a kan abin da muka
sani, muka kuma shaida abin da muka gani ne, amma har yanzu kun ƙi ku karɓi
shaidarmu. 12 Na yi muku magana a kan abubuwan duniya amma ba ku gaskata ba;
to, yaya za ku gaskata in na yi magana a kan abubuwan sama? 13 Ba wanda ya taɓa
hawa zuwa sama sai wanda ya sauka daga sama, wato, Ɗan Mutum.* 14 Kamar dai
yadda Musa ya ɗaga maciji a hamada, haka dole ne a ɗaga Ɗan Mutum, 15 don duk
mai gaskata da shi ya sami rai madawwami.”
16 Gama Allah ya ƙaunaci duniya sosai har ya ba da wanda yake Ɗaya kuma
Makaɗaicin Ɗansa domin duk wanda ya gaskata da shi kada yǎ hallaka sai dai yǎ
sami rai madawwami. 17 Gama Allah bai aiki Ɗansa duniya don yǎ yi wa duniya
hukunci ba, sai dai domin yǎ ceci duniya ta wurinsa. 18 Duk wanda ya gaskata da
shi ba za a yi masa hukunci ba, amma duk wanda bai gaskata ba an riga an yi masa
hukunci domin bai gaskata da sunan wanda yake Ɗaya kuma Makaɗaicin Ɗan Allah
ba. 19 Hukuncin shi ne, Haske ya zo cikin duniya, amma mutane suka so duhu a
maimakon haske domin ayyukansu mugaye ne. 20 Duk mai aikata mugunta yana
ƙin haske, ba zai kuwa zo cikin haske ba don yana tsoro kada ayyukansa su tonu.
21 Amma duk mai rayuwa bisa ga gaskiya yakan zo cikin haske, domin a gani a sarari
cewa ayyukan da ya yi an yi su ne ta wurin Allah.

### *Shaidar Yohanna Mai Baftisma a kan Yesu*

22 Bayan wannan, Yesu da almajiransa suka tafi ƙauyukan Yahudiya, inda ya ɗan
jima da su, ya kuma yi baftisma. 23 To, Yohanna ma yana yin baftisma a Ainon kusa
da Salim, saboda akwai ruwa da yawa a can, mutane kuwa suka yi ta zuwa don a yi
musu baftisma. 24 (Wannan kuwa kafin a sa Yohanna a kurkuku.) 25 Sai gardama ta
tashi tsakanin waɗansu almajiran Yohanna da wani mutumin Yahuda† a kan zancen
al’adar tsarkakewa. 26 Sai suka zo wurin Yohanna suka ce masa, “Rabbi, wancan
mutumin da yake tare da kai a ƙetaren Urdun, wannan da ka ba da shaida a kansa
sosai nan, yana baftisma, kuma kowa yana zuwa wurinsa.”
27 Ga wannan zancen Yohanna ya amsa ya ce, “Mutum yakan karɓi kawai abin da
aka ba shi ne daga sama. 28 Ku kanku za ku shaida cewa na ce, ‘Ba ni ne Kiristi ba,
sai dai an aiko ni ne in sha gabansa.’ 29 Ango ne mai amarya. Abokin da yake masa
hidima yakan jira ya kuma saurara masa, yakan kuma cika da farin ciki sa’ad da ya
ji muryar ango. Wannan farin cikin kuwa nawa ne, ya kuma cika a yanzu. 30 Dole
ne yǎ yi ta ƙaruwa, ni kuma in yi ta raguwa.
31 “Wannan da ya zo daga sama ya fi kowa; wannan da ya zo daga ƙasa na ƙasa ne,
yana kuma magana kamar wanda ya zo daga ƙasa ne. Wannan da ya zo daga sama

* **3:13** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da Mutum, wanda yake cikin sama † **3:25** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da da waɗansu Yahudawa

ya fi kowa. 32 Yana ba da shaidar abin da ya gani da kuma ya ji, duk da haka ba wanda
ya yarda da shaidarsa. 33 Mutumin da ya yarda da ita ya tabbatar da cewa Allah mai
gaskiya ne. 34 Gama wannan da Allah ya aiko yakan faɗi kalmomin Allah ne, gama
Allah yana ba da Ruhu babu iyaka. 35 Uban yana ƙaunar Ɗan ya kuma danƙa kome
a hannuwansa. 36 Duk wanda ya gaskata da Ɗan yana da rai madawwami, amma
duk wanda ya ƙi Ɗan ba zai sami rai ba, gama fushin Allah yana nan a bisansa."

# 4

*Yesu da wata mutuniyar Samariya*

1 Yesu ya ji labari cewa Yahudawa sun ji cewa ya wuce Yohanna samun masu bi,
yana kuma yin musu baftisma, 2 ko da yake ba Yesu ne yake baftismar ba, almajiransa
ne. 3 Da ya sami wannan labari, sai ya bar Yahudiya ya sāke koma Galili.

4 To, ya zama dole yă bi ta Samariya. 5 Sai ya zo wani gari a Samariya da ake ce
da shi Saikar, kurkusa da filin da Yaƙub ya ba wa ɗansa Yusuf. 6 Rijiyar Yaƙub kuwa
tana can, Yesu kuwa, saboda gajiyar tafiya, sai ya zauna a bakin rijiyar. Wajen sa'a
ta shida ne.

7 Sa'ad da wata mutuniyar Samariya ta zo ɗiban ruwa, sai Yesu ya ce mata, "Ba ni
ruwa in sha?" 8 (Almajiransa kuwa sun shiga gari don sayi abinci.)

9 Sai mutuniyar Samariyar ta ce masa, "Kai mutumin Yahuda ne, ni kuwa
mutuniyar Samariya ce. Yaya za ka roƙe ni ruwan sha?" (Don Yahudawa ba sa
hulɗa da Samariyawa.)

10 Yesu ya amsa mata ya ce, "Da kin san kyautar Allah, da kuma wanda yake roƙonki
ruwan sha, da kin roƙe shi, shi kuwa da ya ba ki ruwan rai."

11 Sai macen ta ce, "Ranka yă daɗe, ba ka da guga rijiyar kuwa tana da zurfi. Ina za
ka sami wannan ruwan rai? 12 Ka fi mahaifinmu Yaƙub ne, wanda ya ba mu rijiyar
ya kuma sha daga ciki da kansa, haka ma 'ya'yansa da kuma garkunan shanunsa da
tumakinsa?"

13 Yesu ya amsa ya ce, "Kowa ya sha wannan ruwa, zai sāke jin ƙishirwa, 14 amma
duk wanda ya sha ruwan da zan ba shi, ba zai ƙara jin ƙishirwa ba. Tabbatacce,
ruwan da zan ba shi, zai zama masa maɓuɓɓugan ruwa da yake ɓuɓɓugowa har yă
zuwa rai madawwami."

15 Sai macen ta ce masa, "Ranka yă daɗe, ka ba ni ruwan nan, don kada in ƙara
jin ƙishirwa, in yi ta zuwa nan ɗiban ruwa."

16 Sai ya ce mata, "Je ki zo da mijinki."

17 Sai ta amsa ta ce, "Ai, ba ni da miji."

Yesu ya ce mata, "Gaskiyarki da kika ce ba ki da miji. 18 Gaskiyar ita ce, kin auri
maza biyar, wanda kuke tare yanzu kuwa ba mijinki ba ne. A nan kam kin yi gaskiya."

19 Sai macen ta ce, "Ranka yă daɗe, ina gani kai annabi ne. 20 Kakanninmu sun
yi sujada a dutsen nan, amma ku Yahudawa kun ce a Urushalima ne ya kamata a yi
sujada."

21 Sai Yesu ya ce, "Uwargida, ina tabbatar miki, lokaci yana zuwa da ba za ku yi wa
Uba sujada ko a dutsen nan, ko kuwa a Urushalima ba. 22 Ku Samariyawa ba ku san
abin da kuke yi wa sujada ba; mu kuwa mun san abin da muke yi wa sujada, gama
ceto daga Yahudawa yake. 23 Duk da haka, lokaci yana zuwa har ma ya riga ya yi, da
masu sujada na gaskiya za su yi wa Uba sujada a Ruhu da kuma gaskiya, gama irin
waɗannan masu sujada ne Uba yake nema. 24 Allah ruhu ne, masu yi masa sujada
kuwa dole su yi masa sujada a ruhu, da gaskiya kuma."

25 Macen ta ce, "Na san cewa Almasihu" (da ake ce da shi Kiristi) "yana zuwa. Sa'ad
da ya zo kuwa, zai bayyana mana kome."

26 Sai Yesu ya ce, "Ni mai maganan nan da ke, Ni ne shi."

### *Almajirai sun dawo inda suka bar Yesu*

27 Suna gama magana ke nan sai almajiransa suka iso, suka yi mamakin ganin yana
magana da mace. Amma ba wanda ya ce, “Me kake so?” Ko “Me ya sa kake magana
da ita?”
28 Sai macen ta bar tulunta na ruwa, ta koma cikin gari ta ce wa mutane, 29 “Ku
zo, ku ga mutumin da ya gaya mini duk abin da na taɓa yi. Shin, ko shi ne Kiristi?”
30 Sai suka fita daga garin suka nufa inda yake.
31 Ana cikin haka, sai almajiransa suka roƙe shi suka ce, “Rabbi, ci abinci mana.”
32 Amma ya ce musu, “Ina da abincin da ba ku san kome a kai ba.”
33 Sai almajiran suka ce wa juna, “Shin, ko wani ya kawo masa abinci ne?”
34 Yesu ya ce, “Abincina shi ne, in aikata nufin wannan da ya aiko ni, in kuma gama
aikinsa. 35 Ba kukan ce, ‘Sauran wata huɗu a yi girbi ba?’ Ina gaya muku, ku ɗaga
idanu ku dubi gonaki! Sun isa girbi. 36 Mai girbi na samun lada, yana kuma tara
amfani zuwa rai madawwami, domin mai shuka da mai girbi su yi farin ciki tare.
37 Karin maganan nan gaskiya ne cewa, ‘Wani da shuka, wani kuma da girbi.’ 38 Na
aike ku girbin abin da ba ku yi aikinsa ba. Waɗansu sun yi aikin nan mai wahala,
ku kuwa kun sami ladan aikinsu.”

### *Samariyawa da yawa sun ba da gaskiya*

39 Samariyawa da yawa daga wannan gari suka gaskata da shi saboda shaidar
macen da ta ce, “Ya gaya mini duk abin da na taɓa yi.” 40 To, da Samariyawa suka
zo wurinsa, sai suka roƙe shi yǎ zauna da su, ya kuwa zauna kwana biyu. 41 Saboda
kalmominsa kuwa da yawa suka gaskata.
42 Sai suka ce wa macen, “Yanzu kam mun gaskata, ba don abin da kika faɗa kawai
ba; yanzu mun ji da kanmu, mun kuwa san cewa wannan mutum tabbatacce shi ne
Mai Ceton duniya.”

### *Yesu ya warkar da ɗan mai mulki*
### *(Mattiyu 8.5-13; Luka 7.1-10)*

43 Bayan kwana biyun nan sai ya bar can zuwa Galili. 44 (To, Yesu kansa ya taɓa
faɗa cewa annabi ba shi da daraja a ƙasarsa.) 45 Da ya isa Galili, sai mutanen Galili
suka marabce shi. Sun ga duk abin da ya yi a Urushalima a lokacin Bikin Ketarewa,
gama su ma sun kasance a can.
46 Sai ya sāke ziyarci Kana ta Galili inda ya juya ruwa ya zama ruwan inabi.
Akwai wani ma’aikacin hukuma a can wanda ɗansa yake kwance da rashin lafiya a
Kafarnahum. 47 Da mutumin nan ya ji cewa Yesu ya isa Galili daga Yahudiya, sai ya
je wurinsa ya roƙe shi yǎ zo yǎ warkar da ɗansa da yake bakin mutuwa.
48 Yesu ya ce masa, “Ku mutane, in ba kun ga alamu da abubuwan banmamaki ba,
ba yadda za a yi ku ba da gaskiya.”
49 Ma’aikacin hukuman ya ce, “Ranka yǎ daɗe, ka zo kafin ɗana yǎ mutu.”
50 Sai Yesu ya amsa ya ce, “Ka tafi. Ɗanka zai rayu.”
Mutumin kuwa ya amince da maganar da Yesu ya yi ya kuwa tafi. 51 Tun yana kan
hanya, bayinsa suka tarye shi da labari cewa yaron yana warkewa. 52 Da ya tambayi
lokacin da ɗansa ya sami sauƙi, sai suka ce masa, “Zazzaɓin ya sake shi jiya a sa’a
ta bakwai.”
53 Sai mahaifin ya gane a daidai wannan lokaci ne Yesu ya ce masa, “Ɗanka zai
rayu.” Saboda haka shi da dukan iyalinsa suka gaskata.
54 Wannan ce abin banmamaki ta biyu da Yesu ya yi, bayan zuwansa daga Yahudiya
zuwa Galili.

# 5

### *Warkarwa a tafki*

1 Bayan an ɗan jima, sai Yesu ya haura zuwa Urushalima don wani bikin Yahudawa.
2 To, a Urushalima akwai wani tafki kusa da Kofar Tumaki, wanda a yaren Arameyik
ake kira Betesda[*] an kuma kewaye shi da shirayi biyar. 3 A nan naƙasassu da yawa
sukan kwanta, makafi, guragu, shanyayyu.[†] 5 Akwai wani da yake nan ba shi da
amfani shekara talatin da takwas. 6 Da Yesu ya gan shi kwance a can ya kuma sami
labari cewa ya daɗe a wannan hali, sai ya tambaye shi, "Kana so ka warke?"
7 Marar amfanin nan ya ce, "Ranka yă daɗe, ba ni da wanda zai taimaka yă sa ni a
cikin tafkin sa'ad da aka motsa ruwan. Yayinda nake ƙoƙarin shiga, sai wani yă riga
ni."
8 Sai Yesu ya ce masa, "Tashi! Ɗauki tabarmarka ka yi tafiya." 9 Nan take mutumin
ya warke; ya ɗauki tabarmarsa ya yi tafiya.
A ranar da wannan ya faru ranar Asabbaci ce, 10 saboda haka kuwa Yahudawa suka
ce wa mutumin da aka warkar, "Yau Asabbaci ne; doka ta hana ka ɗauki tabarmarka."
11 Amma ya amsa ya ce, "Mutumin da ya warkar da ni shi ya ce mini, 'Ɗauki
tabarmarka ka yi tafiya.' "
12 Sai suka tambaye shi suka ce, "Wane ne wannan da ya ce maka ka ɗauke ta ka
yi tafiya?"
13 Mutumin da aka warkar kuwa bai ma san ko wane ne ba ne, gama Yesu ya ɓace
cikin taron da yake can.
14 Daga baya Yesu ya same shi a haikali ya ce masa, "Ga shi, ka warke. Ka daina
yin zunubi, in ba haka ba wani abin da ya fi wannan muni zai iya samunka." 15 Sai
mutumin ya je ya gaya wa Yahudawa cewa Yesu ne ya warkar da shi.

### *Rai ta wurin Ɗan*

16 To, domin Yesu yana yin waɗannan abubuwa a ranar Asabbaci, sai Yahudawa
suka tsananta masa. 17 Yesu ya ce musu, "Ubana yana cikin aikinsa kullum har yă
zuwa wannan rana, haka ni ma, ina kan aiki." 18 Don haka Yahudawa suka ƙara
nema su kashe shi; ba don yă karya Asabbaci kawai ba, har ma yana ce Allah Ubansa
ne, yana mai da kansa daidai da Allah.
19 Sai Yesu ya ba su wannan amsa cewa, "Gaskiya nake gaya muku, Ɗan ba ya
iya yin kome da kansa; yana yin abin da ya ga Ubansa yake yi ne kawai, gama duk
abin da Uban yake yi shi ne Ɗan ma yake yi. 20 Gama Uban yana ƙaunar Ɗan yana
kuma nuna masa duk abin da yake yi. I, za ku kuwa yi mamaki, gama zai nuna
masa abubuwan da suka fi waɗannan girma. 21 Gama kamar yadda Uban yake tā
da matattu yake kuma ba su rai, haka ma Ɗan yake ba da rai ga wanda ya ga dama.
22 Bugu da ƙari, Uban ba ya hukunta kowa, sai dai ya danƙa dukan hukunci a hannun
Ɗan, 23 don kowa yă girmama Ɗan kamar yadda yake girmama Uban. Wanda ba ya
girmama Ɗan ba ya girmama Uban, da ya aiko shi ke nan.
24 "Gaskiya nake gaya muku, duk wanda ya ji maganata ya kuma gaskata da wanda
ya aiko ni yana da rai madawwami ba za a kuma hukunta shi ba; ya riga ya ƙetare
daga mutuwa zuwa rai. 25 Gaskiya nake gaya muku, lokaci yana zuwa har ma ya riga
ya zo sa'ad da matattu za su ji muryar Ɗan Allah waɗanda kuwa suka ji za su rayu.
26 Gama kamar yadda Uban yana da rai a cikinsa, haka ya sa Ɗan yă kasance da rai
a cikin kansa. 27 Ya kuma ba shi iko yă hukunta domin shi Ɗan Mutum ne.

---

[*] **5:2** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da Betzata; waɗansu kuma suna da Betsaida ne a nan. [†] **5:3** Waɗansu rubuce-rubucen hannu marar muhimmanci sosai suna da shanyayyu, kuma suka jira a motsa ruwaye. 4 Lokaci-lokaci mala'ikan Ubangiji yakan sauko ya motsa ruwaye. Mutum na farko da ya shiga tafkin bayan motsawa zai warke daga kowace cutar da yake da ita.

28 “Kada ku yi mamakin wannan, gama lokaci yana zuwa da duk waɗanda suke
cikin kaburbura za su ji muryarsa 29 su kuma fito, waɗanda suka aikata nagarta za su
tashi zuwa ga rai, waɗanda kuma suka aikata mugunta za su tashi zuwa ga hukunci.
30 Ni kaɗai dai ba na iya yin kome, ina shari’a ne bisa ga abin da na ji. Shari’ata kuwa
mai adalci ce. Gama ba na neman gamsar da kaina, sai dai in gamshi shi wanda ya
aiko ni.

### *Shaidu game da Yesu*

31 “In na ba da shaida a kaina, shaidata ba gaskiya ba ce. 32 Akwai wani mai ba da
shaida mai kyau a kaina, na kuma san cewa shaidarsa game da ni gaskiya ce.
33 “Kun aika wajen Yohanna ya kuma yi shaida a kan gaskiya. 34 Ba cewa ina neman
shaidar mutum ba ne; sai dai na faɗi haka ne domin ku sami ceto. 35 Yohanna fitila
ne da ya ci ya kuma ba da haske, kun kuwa zaɓa ku ji daɗin haskensa na ɗan lokaci.
36 “Ina da shaidar da ta fi ta Yohanna ƙarfi. Gama aikin nan da Uba ya ba ni in
kammala, wanda kuwa nake yi, yana ba da shaida cewa Uba ne ya aiko ni. 37 Uba
da ya aiko ni kuwa kansa ya yi shaida game da ni. Ba ku taɓa jin muryarsa ko ganin
siffarsa ba, 38 maganarsa kuwa ba ta zama a cikinku, gama ba ku gaskata da wanda
ya aiko ni ba. 39 Kuna ta nazarin Nassosi da himma don kuna tsammani ta wurinsu
ne kuna samun rai madawwami. Nassosin nan ne suke ba da shaida a kaina, 40 duk
da haka kun ƙi zuwa wurina domin ku sami rai.
41 “Ni ba na neman yabon mutane, 42 na fa san ku. Na san cewa ba ku da ƙaunar
Allah a cikin zukatanku. 43 Na zo a cikin sunan Ubana, ba ku kuwa karɓe ni ba;
amma a ce wani dabam ya zo a cikin sunan kansa, za ku karɓe shi. 44 Ta yaya za ku
gaskata in kuna neman yabon junanku, ba kwa kuwa yin ƙoƙarin neman yabon da
yake zuwa daga Allah Makaɗaici?
45 “Kada fa ku yi tsammani zan yi ƙararku wurin Uba. Akwai mai yin ƙararku, shi
ne Musa, wanda kuke dogara da shi. 46 Da a ce kun gaskata da Musa, da kun gaskata
ni, domin ya rubuta game da ni. 47 Amma da yake ba ku gaskata abin da ya rubuta
ba, yaya za ku gaskata maganata?”

# 6

### *Yesu ya ciyar da dubu biyar*
### *(Mattiyu 14.13-21; Markus 6.30-44; Luka 9.10-17)*

1 Ɗan lokaci bayan wannan, sai Yesu ya ƙetare zuwa gaɓar mai nesa na Tekun
Galili (wato, Tekun Tibariya), 2 sai taro mai yawa na mutane suka bi shi domin sun
ga abubuwan banmamakin da ya yi ga marasa lafiya. 3 Sa’an nan Yesu ya hau gefen
dutse ya zauna tare da almajiransa. 4 Bikin Ketarewan Yahudawa ya yi kusa.
5 Sa’ad da Yesu ya ɗaga kai ya ga taro mai yawa suna zuwa wajensa, sai ya ce wa
Filibus, “Ina za mu sayi burodi saboda mutanen nan su ci?” 6 Ya yi wannan tambayar
don yǎ gwada shi ne kawai, gama ya riga ya san abin da zai yi.
7 Sai Filibus ya amsa ya ce, “Kai, ko albashin wata takwas ba zai iya sayan isashen
burodin da kowa zai ɗan samu kaɗan ba!”
8 Sai wani daga cikin almajiransa Andarawus, ɗan’uwan Bitrus, ya yi magana, 9 “Ga
wani yaro da ƙananan burodin sha’ir guda biyar da ƙananan kifi biyu, amma me
wannan zai yi wa yawan mutanen nan.”
10 Yesu ya ce, “Ku sa mutanen su zauna.” Wurin kuwa akwai ciyawa da sosai, sai
maza suka zazzauna, sun kai wajen dubu biyar. 11 Sa’an nan Yesu ya ɗauki burodin,
ya yi godiya, ya kuma rarraba wa waɗanda suke zaune gwargwadon abin da ya ishe
su. Haka kuma ya yi da kifin.
12 Sa’ad da duk suka ci suka ƙoshi, sai ya ce wa almajiransa, “Ku tattara gutsattsarin
da suka rage. Kada kome yǎ lalace.” 13 Saboda haka suka tattara su suka kuma cika

kwanduna goma sha biyu na gutsattsarin burodin sha'ir biyar nan da suka ragu
bayan kowa ya ci.
14 Bayan mutanen suka ga abin banmamakin da Yesu ya yi, sai suka fara cewa,
"Lalle, wannan shi ne Annabin nan mai zuwa duniya." 15 Da Yesu ya gane suna
shirin su ɗauke shi ƙarfi da yaji su naɗa shi sarki, sai ya sāke komawa kan dutsen
shi kaɗai.

### *Yesu ya yi tafiya a kan ruwa*
### *(Mattiyu 14.22-27; Markus 6.45-52)*

16 Da yamma ta yi, sai almajiransa suka gangara zuwa tafki, 17 inda suka shiga jirgin
ruwa suka tasar wa haye tafkin zuwa Kafarnahum. A lokacin kuwa duhu ya yi, Yesu
kuma bai riga ya zo wurinsu ba tukuna. 18 Iska mai ƙarfi kuwa tana bugowa, ruwaye
kuma suka fara hauka. 19 Bayan sun yi tuƙi wajen mil uku ko uku da rabi, sai suka
ga Yesu ya kusato jirgin ruwan, yana takawa a kan ruwan; sai suka tsorata. 20 Amma
ya ce musu, "Ni ne; kada ku ji tsoro." 21 Sa'an nan suka yarda suka karɓe shi a cikin
jirgin ruwan, nan da nan kuwa jirgin ya kai gaɓar da za su.
22 Kashegari taron da suka tsaya a wancan ƙetaren tafkin suka lura cewa jirgin
ruwa ɗaya ne yake a can dā ma, kuma sun lura cewa Yesu bai shiga ciki tare da
almajiransa ba, gama sun tashi su kaɗai. 23 Sai ga waɗansu jiragen ruwa daga
Tibariya suka iso kusa da wurin da mutanen suka ci burodi bayan Ubangiji ya yi
godiya. 24 Da taron suka lura cewa Yesu da almajiransa ba sa can, sai suka shiga
jiragen ruwa suka tafi Kafarnahum neman Yesu.

### *Yesu burodin rai*

25 Da suka same shi a wancan ƙetaren tafkin, sai suka tambaye shi suka ce, "Rabbi,
yaushe ka kai nan?"
26 Yesu ya amsa ya ce, "Gaskiya nake gaya muku, kuna nemana ne ba don kun ga
abubuwan banmamaki ba, sai dai domin kun ci burodi kun ƙoshi. 27 Kada ku yi aiki
saboda abincin da yake lalacewa, sai dai saboda abinci mai dawwama har yă zuwa
rai madawwami, wanda Ɗan Mutum zai ba ku. A kansa ne Allah Uba ya sa hatimin
amincewarsa."
28 Sai suka tambaye shi suka ce, "Me za mu yi don mu aikata ayyukan da Allah
yake so?"
29 Yesu ya amsa, "Aikin Allah shi ne, a gaskata da wanda ya aiko."
30 Sai suka tambaye shi, "Wace abin banmamaki ce za ka yi don mu gani mu kuwa
gaskata ka? Me za ka yi? 31 Kakannin-kakanninmu sun ci Manna a hamada; kamar
yadda yake a rubuce, 'Ya ba su burodi daga sama su ci.'*"
32 Yesu ya ce musu, "Gaskiya nake gaya muku, ba Musa ne ya ba ku burodi daga
sama ba, sai dai Ubana ne yake ba ku burodi na gaskiya daga sama. 33 Gama burodin
Allah shi ne wanda yake saukowa daga sama, yana kuma ba wa duniya rai."
34 Sai suka ce, "Ranka yă daɗe, daga yanzu ka dinga ba mu wannan burodi."
35 Sa'an nan Yesu ya furta cewa, "Ni ne burodin rai. Wanda ya zo wurina ba
zai taɓa jin yunwa ba, wanda kuma ya gaskata da ni ba zai taɓa jin ƙishirwa ba.
36 Amma kamar yadda na faɗa muku, kun gan ni duk da haka ba ku gaskata ba.
37 Duk waɗanda Uba ya ba ni za su zo wurina, kuma duk wanda ya zo wurina ba
zan kore shi ba ko kaɗan. 38 Gama na sauko daga sama ba don in cika nufin kaina
ba sai dai don in cika nufin shi wanda ya aiko ni. 39 Nufin wanda ya aiko ni kuwa
shi ne, kada in yar da ko ɗaya daga cikin duk waɗanda ya ba ni, sai dai in tashe su a
rana ta ƙarshe. 40 Gama nufin Ubana shi ne, duk wanda yake duban Ɗan, ya kuma
gaskata shi zai sami rai madawwami, ni kuwa zan tashe shi a rana ta ƙarshe."

* **6:31** Fit 16.4; Neh 9.15; Zab 78.24,25

41 Da jin haka, Yahudawa suka fara gunaguni a kansa, domin ya ce, “Ni ne burodin
da ya sauka daga sama.” 42 Suka ce, “Kai, wannan ba Yesu ba ne, ɗan Yusuf, wanda
mahaifinsa da mahaifiyarsa duk mun san su? Yaya yanzu zai ce, ‘Na sauko daga
sama?’ ”
43 Sai Yesu ya amsa ya ce, “Ku daina gunaguni a junanku. 44 Ba mai iya zuwa
wurina, sai dai in Uban da ya aiko ni ya jawo shi, ni kuwa zan tashe shi a rana ta
ƙarshe. 45 A rubuce yake a cikin Annabawa cewa, ‘Allah zai koyar da dukansu.’†Duk
wanda ya saurari Uba, ya kuma koyi daga wurinsa, zai zo wurina. 46 Ba wanda ya
taɓa ganin Uban, sai shi wanda ya zo daga Allah; shi ne kaɗai ya taɓa ganin Uban.
47 Gaskiya nake gaya muku, wanda ya gaskata yana da rai madawwami. 48 Ni ne
burodin rai. 49 Kakannin-kakanninku sun ci Manna a hamada, duk da haka suka
mutu. 50 Amma ga burodin da ya sauko daga sama, wanda mutum zai iya ci, ba
zai kuma mutu ba. 51 Ni ne burodin rai mai saukowa daga sama. Duk wanda ya ci
wannan burodi, zai rayu har abada. Wannan burodin shi ne jikina, da zan bayar don
duniya ta sami rai.”
52 Sai Yahudawa suka fara gardama mai tsanani a junansu suna cewa, “Yaya
wannan mutum zai ba mu naman jikinsa mu ci?”
53 Sai Yesu ya ce musu, “Gaskiya nake gaya muku, sai kun ci naman jikin Ɗan
Mutum kuka kuma sha jininsa, ba za ku kasance da rai a cikinku ba. 54 Duk wanda
ya ci naman jikina ya kuma sha jinina, yana da rai madawwami. Ni kuwa zan tashe
shi a rana ta ƙarshe. 55 Gama naman jikina abinci ne na gaskiya jinina kuma abin
sha ne na gaskiya. 56 Duk wanda ya ci naman jikina ya kuma sha jinina, yana cikina,
ni kuma ina cikinsa. 57 Kamar dai yadda Uba mai rai ya aiko ni, ina kuma rayuwa
ta saboda shi, haka ma wanda yake ni ne abincinsa zai rayu saboda ni. 58 Wannan
shi ne burodin da ya sauko daga sama. Kakannin-kakanninku sun ci Manna suka
kuma mutu, amma duk wanda yake cin wannan burodi zai rayu har abada.” 59 Ya
faɗi wannan ne lokacin da yake koyarwa a cikin majami’a a Kafarnahum.

### *Almajirai masu yawa sun bar bin Yesu*

60 Da jin haka, da yawa daga cikin almajiransa suka ce, “Wannan koyarwa tana da
wuya. Wa zai iya yarda da ita?”
61 Da yake ya san almajiransa suna gunaguni game da wannan, sai Yesu ya ce
musu, “Wannan ya ɓata muku rai ne? 62 Me za ku ce ke nan, in kuka gan Ɗan
Mutum yana hawa zuwa inda yake dā! 63 Ruhu ne yake ba da rai; jikin kam, ba ya
amfana kome. Kalmomin da na faɗa muku, Ruhu ne, da kuma rai. 64 Duk da haka
akwai waɗansunku da ba su gaskata ba.” Gama Yesu ya sani tun farko, waɗanda ba
su gaskata ba, da kuma wanda zai bashe shi. 65 Ya ci gaba da cewa, “Shi ya sa na
faɗa muku cewa ba mai iya zuwa wurina, sai dai Uba ya yardar masa.”
66 Daga wannan lokaci da yawa daga cikin almajiransa suka ja da baya, suka daina
bin sa.
67 Sai Yesu ya tambayi Sha Biyun, “Ku ma za ku tafi ne?”
68 Sai Siman Bitrus ya amsa ya ce, “Ubangiji wajen wa za mu tafi? Kai ne da
kalmomin rai madawwami. 69 Mun gaskata mun kuma san cewa kai ne Mai Tsarkin
nan na Allah.”
70 Sai Yesu ya amsa ya ce, “Ba ni na zaɓe ku Sha Biyu ba? Amma ɗayanku Iblis
ne!” 71 (Yana nufin Yahuda, ɗan Siman Iskariyot, wanda, ko da yake ɗaya ne cikin
Sha Biyun, zai bashe shi daga baya.)

## 7

### *Yesu ya tafi Bikin Tabanakul*

† **6:45** Ish 54.13

1 Bayan wannan, sai Yesu ya yi ta zagawa a cikin Galili, da ganga bai yarda yǎ je
Yahudiya ba domin Yahudawa a can suna nema su kashe shi. 2 Amma sa'ad da Bikin
Tabanakul na Yahudawa ya yi kusa, 3 sai 'yan'uwan Yesu suka ce masa, "Ya kamata
ka bar nan ka tafi Yahudiya, don almajiranka su ga ayyukan banmamaki da kake
yi. 4 Ba wanda yake so a san shi da zai yi abu a ɓoye. Da yake kana yin waɗannan
abubuwa, sai ka nuna kanka ga duniya." 5 Domin ko 'yan'uwansa ma ba su gaskata
da shi ba.
6 Saboda haka Yesu ya ce musu, "Lokacina bai yi ba tukuna; amma a gare ku
kowane lokaci daidai ne. 7 Duniya ba za tǎ iya ƙinku ba, amma ni take ƙi domin ina
shaida cewa ayyukanta mugaye ne. 8 Ku ku tafi Bikin, ba zan haura zuwa wannan
Bikin ba yanzu, domin lokacina bai yi ba tukuna." 9 Da ya faɗa haka, sai ya dakata
a Galili.
10 Amma fa, bayan 'yan'uwansa suka tafi Bikin, shi ma ya tafi, ba a fili ba, amma
a ɓoye. 11 A Bikin kuwa, Yahudawa suka yi ta nemansa, suna cewa, "Ina mutumin
yake?"
12 A cikin taron kuwa aka yi ta raɗe-raɗe game da shi. Waɗansu suka ce, "Shi
mutumin kirki ne."
Waɗansu kuwa suka ce, "A'a, ai, ruɗin mutane yake." 13 Amma ba wanda ya ce
kome a fili game da shi don tsoron Yahudawa.

### *Yesu ya koyar a bikin*

14 Sai bayan da aka kai tsakiyar Bikin, sa'an nan Yesu ya haura zuwa filin haikali
ya fara koyarwa. 15 Yahudawa suka yi mamaki suna tambaya, "Yaya wannan mutum
ya sami wannan sani haka ba tare da ya yi wani karatu ba?"
16 Yesu ya amsa ya ce, "Koyarwata ba tawa ba ce, ta fito ne daga wurin wanda ya
aiko ni. 17 Duk wanda ya zaɓi yin nufin Allah, zai gane ko koyarwata daga Allah ce,
ko kuwa don kaina ne nake magana. 18 Mai magana don kansa, neman ɗaukakar
kansa yake yi. Amma mai neman ɗaukakar wanda ya aiko shi, shi ne mai gaskiya,
ba kuwa rashin gaskiya a gare shi. 19 Ashe, ba Musa ba ne ya ba ku Doka? Duk da
haka ba ko ɗayanku da yake kiyaye Dokar. Me ya sa kuke nema ku kashe ni?"
20 Taron suka amsa suka ce, "Kana da aljani, wane ne yake so yǎ kashe ka?"
21 Yesu ya ce musu, "Na yi abin banmamaki ɗaya, dukanku kuwa kuka yi mamaki.
22 Duk da haka, domin Musa ya bar muku kaciya (ko da yake a gaskiya, ba daga wurin
Musa ne ya fito ba, sai dai daga wurin kakannin kakanninku), ga shi kuna yin wa
yaro kaciya a ranar Asabbaci. 23 To, in za a iya yin wa yaro kaciya a ranar Asabbaci
don kada a karya dokar Musa, don me kuke fushi da ni saboda na warkar da mutum
a ranar Asabbaci? 24 Ku daina yin shari'a bisa ga ganin ido, sai dai ku yi shari'a bisa
ga adalci."

### *Shin, Yesu shi ne Kiristi?*

25 A nan ne fa waɗansu mutane daga Urushalima suka fara tambaya suna cewa,
"Ashe, ba wannan mutum ne suke nema su kashe ba? 26 Ga shi nan yana magana a
fili, su kuma ba su ce masa uffam ba. Ko hukumomi sun yarda cewa shi ne Kiristi?
27 Mun dai san inda mutumin nan ya fito; amma sa'ad da Kiristi ya zo ba wanda zai
san inda ya fito."
28 Yesu yana cikin koyarwa a filin haikali ke nan, sai ya ɗaga murya ya ce, "I, kun
san ni, kun kuma san inda na fito. Ban zo don kaina ba, sai dai shi da ya aiko ni mai
gaskiya ne. Ba ku san shi ba, 29 amma na san shi, domin ni daga wurinsa ne, kuma
shi ya aiko ni."
30 Da jin haka, sai suka yi ƙoƙari su kama shi, sai dai ba wanda ya taɓa shi, don
lokacinsa bai yi ba tukuna. 31 Duk da haka, da yawa a cikin taron suka ba da gaskiya

gare shi. Suka ce, “Sa’ad da Kiristi ya zo, zai yi abubuwan banmamaki fiye da na
wannan mutum ne?”
32 Farisiyawa suka ji taron suna raɗe-raɗen waɗannan abubuwa game da shi. Sai
manyan firistoci da Farisiyawa suka aiki masu gadin haikalin su kama shi.
33 Sai Yesu ya ce, “Ina tare da ku na ɗan ƙanƙanin lokaci ne kawai, sa’an nan zan
koma wurin wanda ya aiko ni. 34 Za ku neme ni, amma ba za ku same ni ba; inda
nake kuwa, ba za ku iya zuwa ba.”
35 Sai Yahudawa suka ce wa juna, “Ina mutumin nan yake niyyar tafiya da ba
za mu iya samunsa ba? Zai je wurin mutanenmu da suke zaune warwatse a cikin
Hellenawa, yǎ kuma koya wa Hellenawa ne? 36 Me yake nufi da ya ce, ‘Za ku neme
ni, amma ba za ku same ni ba,’ da kuma ‘Inda nake, ba za ku iya zuwa ba’?”
37 A rana ta ƙarshe kuma mafi girma ta Bikin, Yesu ya tsaya ya yi magana da babbar
murya ya ce, “Duk mai jin ƙishirwa, yǎ zo wurina yǎ sha. 38 Duk wanda ya gaskata
da ni, kamar yadda Nassi ya ce, kogunan ruwa masu rai za su gudana daga cikinsa.”
39 Da wannan yana nufin Ruhu ke nan, wanda waɗanda suka gaskata da shi za su
karɓa daga baya. Har yǎ zuwa wannan lokaci ba a ba da Ruhu ba tukuna, da yake
ba a riga an ɗaukaka Yesu ba.
40 Da jin kalmominsa, waɗansu mutane suka ce, “Ba shakka, mutumin nan shi ne
Annabin.”
41 Waɗansu suka ce, “Shi ne Kiristi.”
Waɗansu har wa yau suka ce, “Yaya Kiristi zai fito daga Galili? 42 Nassi bai ce Kiristi
zai fito daga zuriyar Dawuda, daga kuma Betlehem garin da Dawuda ya zauna ba?”
43 Sai mutanen suka rabu saboda Yesu. 44 Waɗansu suka so su kama shi, sai dai ba
wanda ya taɓa shi.

### *Rashin bangaskiyar shugabannin Yahudawa*

45 A ƙarshe masu gadin haikali suka koma wurin manyan firistocin da Farisiyawa,
waɗanda suka tambaye su cewa, “Don me ba ku kawo shi nan ba?”
46 Sai masu gadin suka ce, “Kai, babu wanda ya taɓa magana kamar wannan
mutum.”
47 Sai Farisiyawa suka amsa cikin fushi suka ce, “Af, kuna nufi har da ku ma ya
ruɗe ku ke nan? 48 Akwai wani daga cikin masu mulki ko cikin Farisiyawan da ya
gaskata da shi? 49 A’a! Sai dai wannan taron da ba su san kome game da Doka ba,
la’anannu ne.”
50 Nikodimus, wanda ya je wurin Yesu dā, wanda kuma yake ɗayansu ya ce,
51 “Ashe, dokarmu takan hukunta mutum ba tare da an fara ji daga bakinsa game da
abin da yake yi ba?”
52 Sai suka amsa suka ce, “Kai ma daga Galili ne? Bincika ka gani, za ka iske cewa
ba annabin da zai fito daga Galili.”
[Rubuce-rubucen farko-farko da kuma mafi ingancin da aka fi dogara da su tare
da waɗansu shaidu na dā ba su da Yoh 7.53–8.11. Kaɗan daga cikin rubuce-rubucen
hannu na dā sun ƙunshi waɗannan ayoyi, ko gaba ɗayansu ko kuma sashensu kawai
bayan Yoh 7.36, Yoh 21.25, Luk 21.38 ko kuwa Luk 24.53.]
53 *Sai kowannensu ya koma gidansa.*

## 8

1 *Amma Yesu ya tafi Dutsen Zaitun.*
2 *Da sassafe ya sāke bayyana a filin haikali, inda dukan mutane suka taru kewaye da*
*shi, sai ya zauna don yǎ koya musu.* 3 *Sai malaman dokoki da Farisiyawa suka kawo*
*wata macen da aka kama a zina. Suka sa ta tsaya a gaban taron* 4 *suka kuma ce wa*
*Yesu, “Malam, an kama wannan mace tana zina.* 5 *A cikin Doka Musa ya umarce mu,*

*mu jajjefe irin waɗannan mata. To, me ka ce?"* 6 *Sun yi wannan tambaya ce don su sa*
*masa tarko, don su sami hanyar zarge shi.*
*Amma Yesu ya sunkuya ya fara rubutu a ƙasa da yatsarsa.* 7 *Da suka ci gaba da*
*yin masa tambayoyi, sai ya miƙe tsaye ya ce musu, "In da wani a cikinku da ba shi da*
*zunubi, sai yă fara jifanta da dutse."* 8 *Sai ya sāke sunkuyawa ya kuma yi rubutu a*
*ƙasa.*
9 *Da jin haka, waɗanda suka ji sai suka fara tashi daga wurin ɗaya-ɗaya, tun daga*
*babbansu har ya zuwa ƙaraminsu, sai da aka bar Yesu kaɗai, tare da macen tsaye a*
*wurin.* 10 *Sai Yesu ya miƙe tsaye ya tambaye ta ya ce, "Mace, ina suke? Ba wanda ya*
*hukunta ki?"*
11 *Ta ce, "Ba kowa, ranka yă daɗe."*
*Sai Yesu ya ce, "Haka ni ma ban hukunta ki ba. Ki tafi, ki daina rayuwar zunubi."*

### *Gaskiyar shaidar Yesu*

12 Sa'ad da Yesu ya sāke magana da mutanen, sai ya ce, "Ni ne hasken duniya. Duk
wanda ya bi ni ba zai yi tafiya cikin duhu ba, sai dai yă sami hasken rayuwa."
13 Sai Farisiyawa suka tambaye shi suka ce, "Ga kai dai, kana yi wa kanka shaida,
shaidarka kuwa ba tabbatacciya ba ce."
14 Sai Yesu ya amsa ya ce, "Ko na shaidi kaina, ai, shaidata tabbatacciya ce, gama
na san inda na fito da kuma inda za ni. Amma ku ba ku san inda na fito ko inda za
ni ba. 15 Kuna shari'a bisa ga ma'aunin mutane; ni kuwa ba na yin wa kowa shari'a.
16 Amma ko da zan yi shari'a, shari'ata daidai ce, don ba ni kaɗai ba ne. Ina tare
da Uba da ya aiko ni. 17 A cikin Dokarku a rubuce yake cewa shaidar mutum biyu
tabbatacciya ce. 18 Ni ne nake shaidar kaina, Uba da ya aiko ni kuma yana shaidata."
19 Suka tambaye shi suka ce, "Ina Uban nan naka?"
Sai Yesu ya ce, "Ba ku san ni ko Ubana ba. Da kun san ni, da za ku san Ubana ma."
20 Ya faɗi waɗannan kalmomi ne yayinda yake koyarwa a filin haikali, kusa da inda
ake ajiye baye-baye. Duk da haka ba wanda ya kama shi, domin lokacinsa bai yi ba
tukuna.
21 Har wa yau Yesu ya sāke ce musu, "Zan tafi, za ku kuwa neme ni, za ku kuma
mutu cikin zunubinku. Inda za ni, ba za ku iya zuwa ba."
22 Wannan ya sa Yahudawa suka yi tambaya suka ce, "Zai kashe kansa ne? Shi ya
sa yake cewa, 'Inda za ni, ba za ku iya zuwa ba'?"
23 Amma ya ci gaba da cewa, "Ku daga ƙasa kuke; ni kuwa daga bisa ne. Ku na
duniyan nan ne; ni kuwa ba na duniyan nan ba ne. 24 Na gaya muku cewa za ku
mutu cikin zunubanku; in ba ku gaskata cewa ni ne wanda na ce nake ba, lalle za ku
mutu cikin zunubanku."
25 Suka ce, "Wane ne kai?"
Sai Yesu ya amsa ya ce, "Ni ne wannan da na sha faɗi muku. 26 Ina da abubuwa
masu yawa da zan faɗa game ku in kuma yi muku shari'a. Amma wanda ya aiko ni
mai aminci ne, abin da kuma na ji daga gare shi, shi nake gaya wa duniya."
27 Ba su gane cewa yana yin musu magana game da Ubansa ba ne. 28 Saboda haka
Yesu ya ce, "Sa'ad da kuka ɗaga Ɗan Mutum, a sa'an nan ne za ku san cewa ni ne
wannan da na ce nake. Ni kuwa ba na yin kome ni kaɗai, sai in dai faɗi abin da
Uba ya koya mini. 29 Wanda kuwa ya aiko ni yana tare da ni; bai bar ni ni kaɗai ba,
domin kullum ina aikata abin da ya gamshe shi." 30 Sa'ad da yake cikin magana, da
yawa suka ba da gaskiya gare shi.

### *'Ya'yan Ibrahim*

31 Sai Yesu ya ce wa Yahudawan da suka gaskata da shi, "In dai kun riƙe koyarwata,
ku almajiraina ne da gaske. 32 Sa'an nan za ku san gaskiya, gaskiyar kuwa za tă
'yantar da ku."

33 Sai suka amsa masa suka ce, “Ai, mu zuriyar Ibrahim ne kuma ba mu taɓa bauta wa kowa ba. Yaya za ka ce za a ʼyantar da mu?”

34 Yesu ya amsa ya ce, “Gaskiya nake gaya muku, duk mai yin zunubi bawan zunubi
ne. 35 Bawa dai ba shi da wurin zama na ɗinɗinɗin a cikin iyali, amma ɗa na gida
ne har abada. 36 Saboda haka in Ɗan ya ʼyantar da ku, za ku ʼyantu da gaske. 37 Na
dai san ku zuriyar Ibrahim ne. Duk da haka kuna shiri ku kashe ni, don maganata
ba ta da wurin zama a cikinku. 38 Ina faɗi muku abin da na gani a wurin Ubana, ku
kuwa kuna yin abin da kuka ji daga wurin ubanku.”

39 Suka ce, “To, ai, Ibrahim ne mahaifinmu.”

Yesu ya ce, “Da ku ʼyaʼyan Ibrahim ne, da za ku aikata abubuwan da Ibrahim ya
yi. 40 Ga shi kun ƙudura, sai kun kashe ni, ni mutumin da ya faɗa muku gaskiyar da
na ji daga Allah. Ibrahim bai yi irin waɗannan abubuwa ba. 41 Kuna yin abubuwan
da ubanku yake yi ne.”

Suka ce, “Mu fa ba shegu ba ne. Uba guda kaɗai da muke da shi, shi ne Allah kansa.”

### *ʼYaʼyan Iblis*

42 Yesu ya ce musu, “Da Allah ne Ubanku, da kun ƙaunace ni, gama daga Allah na
fito yanzu kuma ga ni nan. Ban zo saboda kaina ba, amma shi ne ya aiko ni. 43 Me ya
sa ba kwa gane da maganata? Don ba kwa iya jin abin da nake faɗi. 44 Ku na ubanku
ne, Iblis, kuna kuwa so ku aikata abin da ubanku yake so. Shi mai kisankai ne tun
farko. Ba ruwansa da gaskiya, gama gaskiya ba ta cikinsa. Yayinda yake ƙarya, yana
yin halinsa ne, gama shi maƙaryaci ne, uban ƙarairayi kuma. 45 Amma domin ina
faɗin gaskiya, ba kwa gaskata! 46 Akwai waninku da zai iya haƙaƙƙewa na taɓa yin
zunubi? In kuwa gaskiya na faɗa, me ya sa ba kwa gaskata ni? 47 Wanda yake na
Allah, yakan ji abin da Allah yake faɗi. Abin da ya sa ba kwa jin sa kuwa shi ne don
ku ba na Allah ba ne.”

### *Shaidar Yesu game da kansa*

48 Yahudawa suka amsa masa suka ce, “Aha, ai, gaskiyarmu da muka ce kai mutumin Samariya ne, kana kuma da aljani.”

49 Yesu ya ce, “Ni ba mai aljani ba ne, ni dai ina girmama Ubana, ku kuwa ba
kwa girmama ni. 50 Ba na nema wa kaina ɗaukaka, amma akwai wani wanda yake
neman mini, shi ne kuma alƙali. 51 Gaskiya nake gaya muku, duk wanda ya kiyaye
maganata, ba zai ɗanɗana mutuwa ba sam.”

52 Da jin haka Yahudawa suka ce, “Tabɗi, yanzu kam mun san kana da aljani!
Ibrahim ya mutu haka ma annabawa, ga shi kana cewa duk wanda ya kiyaye
maganarka ba zai ɗanɗana mutuwa ba sam. 53 Ka fi Ibrahim mahaifinmu ne? Ya
mutu, haka ma annabawa. Wa kake ɗauka kanka ne?”

54 Yesu ya amsa ya ce, “In ma na ɗaukaka kaina, ɗaukakata ba kome ba ce. Ubana,
wanda kuke cewa shi ne Allahnku, shi ne wanda yake ɗaukaka ni. 55 Ko da yake ba
ku san shi ba, ni dai na san shi. In kuwa na ce ban san shi ba, na zama maƙaryaci
kamar ku ke nan, amma na san shi, kuma ina kiyaye maganarsa. 56 Mahaifinku
Ibrahim ya yi farin ciki sosai yǎ sami ganin ranata; ya kuwa gan ta, ya yi murna.”

57 Sai Yahudawa suka ce masa, “Kai, shekarunka har yanzu ba su kai hamsin tukuna ba fa, har ka ga Ibrahim!”

58 Yesu ya amsa ya ce, “Gaskiya nake gaya muku, tun ba a haifi Ibrahim ba, ni ne!”
59 Da jin haka sai suka ɗebo duwatsu don su jajjefe shi, amma Yesu ya ɓuya, ya fita
daga filin haikali.

# 9

### *Yesu ya warkar da mutumin da aka haifa makaho*

1 Da Yesu yana tafiya, sai ya ga wani mutum wanda aka haifa makaho. 2 Sai
almajiransa suka tambaye shi suka ce, "Rabbi, wane ne ya yi zunubi, mutumin ne,
ko iyayensa, da ya sa aka haife shi makaho?"
3 Sai Yesu ya ce, "Ba don mutumin ko iyayensa sun yi zunubi ne ba, sai dai don
a bayyana aikin Allah ne a rayuwarsa. 4 Muddin da sauran rana, dole mu yi aikin
wanda ya aiko ni. Dare yana zuwa, sa'ad da ba wanda zai iya yin aiki. 5 Yayinda ina
a cikin duniya, ni ne hasken duniya."
6 Bayan ya faɗi haka, sai ya tofa miyau a ƙasa, ya kwaɓa laka da miyau ɗin, ya
kuma shafa a idanun mutumin. 7 Ya ce masa, "Je ka, ka wanke a Tafkin Silowam"
(kalman nan tana nufin "Aikakke"). Saboda haka mutumin ya tafi ya wanke, ya kuma
dawo gida yana gani.
8 Maƙwabta da waɗanda suka saba ganinsa dā yana bara, suka ce, "Kai, ba wannan
mutum ne ya saba zama yana bara ba?" 9 Waɗansu suka ce shi mana.

Waɗansu kuwa suka ce, "A'a, ya dai yi kama da shi."

Amma shi ɗin ya ce, "Kwarai kuwa ni ne."

10 Sai suka ce, "To, yaya aka yi idanunka suka buɗe?"

11 Ya amsa ya ce, "Mutumin da ake kira Yesu ne ya kwaɓa laka ya shafa mini a
idanu. Ya ce mini in je Silowam in wanke. Na kuwa tafi, na wanke, sai na sami ganin
gari."

12 Suka tambaye shi suka ce, "Ina mutumin yake?"

Ya ce, "Ban sani ba."

### *Farisiyawa sun bincike warkarwar*

13 Sai suka kawo mutumin da dā yake makaho wurin Farisiyawa. 14 To, a ranar
da Yesu ya kwaɓa laka ya buɗe idanun mutumin ranar Asabbaci ce. 15 Saboda haka
Farisiyawa suka tambaye shi yadda ya sami ganin gari. Mutumin ya amsa, "Ya shafa
laka a idanuna, sai na wanke, ina kuwa gani."
16 Sai waɗansu daga cikin Farisiyawa suka ce, "Mutumin nan ba daga Allah yake
ba, don ba ya kiyaye ranar Asabbaci."

Amma waɗansu suka yi tambaya suka ce, "Yaya mutum mai zunubi zai yi irin
abubuwan banmamaki haka?" Sai ra'ayinsu ya sha bamban.
17 A ƙarshe suka sāke koma ga makahon suka ce, "Kai fa, me ka gani game da shi?
Idanunka ne fa ya buɗe."

Sai mutumin ya ce, "Tab, ai, shi annabi ne."

18 Yahudawa dai ba su yarda cewa dā shi makaho ne ya kuma sami ganin gari ba,
sai da suka kira iyayen mutumin. 19 Suka tambaye su, "Wannan ɗanku ne? Shi ne
wanda kuka ce an haife shi makaho? To, ta yaya yake gani yanzu?"
20 Iyayen suka amsa suka ce, "Mun dai san shi ɗanmu ne, mun kuma san cewa an
haife shi makaho. 21 Sai dai yadda yake gani yanzu, ko kuma wa ya buɗe idanunsa, ba
mu sani ba. Ku tambaye shi. Ai, shi ba yaro ba ne, zai faɗa da bakinsa." 22 Iyayensa
sun faɗa haka ne saboda suna tsoron Yahudawa, gama Yahudawa sun riga sun yanke
shawara cewa duk wanda ya yarda cewa Yesu shi ne Kiristi, za a kore shi daga
majami'a. 23 Shi ya sa iyayensa suka ce, "Ai, shi ba yaro ba ne, ku tambaye shi."
24 Sai suka sāke kiran mutumin nan da yake makaho a dā, suka ce masa, "Ka
ɗaukaka Allah, mu kam, mun san mutumin nan mai zunubi ne."
25 Sai ya amsa ya ce, "Ko shi mai zunubi ne ko babu, ni dai ban sani ba. Abu ɗaya
fa na sani, dā ni makaho ne, amma yanzu ina gani!"
26 Sai suka tambaye suka ce, "Shin, me ya yi maka? Ta yaya ya buɗe idanunka?"

27 Ya amsa ya ce, “Na riga na gaya muku ba ku kuwa saurara ba. Don me kuke so
ku sāke ji? Ko ku ma kuna so ku zama almajiransa ne?”
28 Sai suka hau shi da zagi suna cewa, “Kai ne dai almajirin mutumin! Mu almajiran
Musa ne! 29 Mun dai san cewa Allah ya yi magana da Musa, amma wannan mutum
ba mu san inda ya fito ba.”
30 Sai mutumin ya ce, “Cabɗi, yau ga abin mamaki! Ba ku san inda ya fito ba, ga shi
kuwa ya buɗe idanuna. 31 Mun san cewa Allah ba ya sauraron masu zunubi. Yakan
saurari mai tsoronsa mai aikata nufinsa. 32 Ba wanda ya taɓa ji cewa an buɗe idanun
wanda aka haifa makaho. 33 Da mutumin nan ba daga Allah ba ne, da ba abin da zai
iya yi.”
34 Sai suka amsa suka ce, “Kai da aka haifa cike da zunubi; za ka yi karambanin
koyarwar da mu!” Sai suka kore shi.

*Makanta ta ruhaniya*

35 Yesu ya ji labari cewa sun kore shi, da ya same shi kuwa, sai ya ce, “Ka gaskata
da Ɗan Mutum?”
36 Sai mutumin ya amsa ya ce, “Ranka yă daɗe, wane ne shi? Gaya mini, don in
gaskata da shi.”
37 Yesu ya ce, “Yanzu ka gan shi; tabbatacce ma, shi ne yake magana da kai.”
38 Sai mutumin ya ce, “Ubangiji, na gaskata,” ya kuma yi masa sujada.
39 Yesu ya ce, “Saboda shari’a ce na zo duniya nan, saboda makafi su sami ganin
gari, waɗanda suke gani kuma su makance.”
40 Da Farisiyawan da suke tare da shi suka ji ya faɗi haka sai suka yi tambaya suka
ce, “Mene? Mu ma makafi ne?”
41 Yesu ya ce, “Ai, da ku makafi ne ma, da ba ku da zunubi, amma da yake kun ce,
kuna gani, zunubanku suna nan daram.

# 10

*Makiyayi da garkensa*

1 “Gaskiya nake gaya muku, mutumin da bai shiga inda ake ajiye garken tumaki
ta ƙofa ba, amma ya hau ta katanga, ɓarawo ne, ɗan fashi kuma. 2 Mutumin da ya
shiga ta ƙofa makiyayin tumakinsa ne. 3 Mai gadin yakan buɗe wa makiyayin ƙofa,
tumakin kuma sukan saurari muryarsa. Yakan kira tumakinsa da suna, yă kuma fid
da su waje. 4 Sa’ad da ya fitar da dukan nasa waje, sai ya ja gabansu, tumakinsa
kuma sukan bi shi domin sun san muryarsa. 5 Amma ba za su taɓa bin baƙo ba; sai
dai ma su guje masa don ba su san muryar baƙo ba.” 6 Yesu ya yi musu wannan
misali, amma ba su fahimci abin da yake faɗa musu ba.
7 Saboda haka Yesu ya sāke cewa, “Gaskiya nake gaya muku, ni ne ƙofar tumakin.
8 Duk waɗanda suka riga ni zuwa ɓarayi ne, ’yan fashi kuma, amma tumakin ba
su saurare su ba. 9 Ni ne ƙofar; duk wanda ya shiga ta wurina zai sami ceto. Zai
riƙa shiga yă fita yă kuwa sami wurin kiwo. 10 Ɓarawo yakan zo don yă yi sata ne
kawai da kisa da kuma ɓarna. Ni kuwa na zo ne don su sami rai, su kuma same shi
a yalwace.
11 “Ni ne makiyayi mai kyau. Makiyayi mai kyau yakan ba da ransa domin tumakin.
12 Wanda aka ɗauko haya ba shi ne makiyayi mai tumakin ba. Saboda haka sa’ad da
ya ga kyarkeci yana zuwa, sai yă sheƙa da gudu yă bar tumakin. Sai kyarkecin yă kai
wa garken hari, yă kuma watsar da su. 13 Mutumin yakan gudu don shi ɗan haya ne
kawai, bai kuwa damu da tumakin ba.
14 “Ni ne makiyayi mai kyau; na san tumakina, tumakina kuma sun san ni, 15 kamar
yadda Uba ya san ni, ni kuma na san Uba, ina kuwa ba da raina domin tumakin. 16 Ina

da waɗansu tumaki da ba na wannan garken ba ne. Dole ne in kawo su su ma. Za
su saurari muryata, za su kasance garke guda ɗaya, makiyayi guda kuma. [17] Abin da
ya sa Ubana yake ƙaunata ke nan, domin ina ba da raina, in ɗauko shi kuma. [18] Ba
mai karɓe mini rai, ina dai ba da shi. Ina da iko in ba da shi, ina da iko in ɗauko shi
kuma. Wannan umarni kuwa daga wurin Ubana na karɓo shi."

[19] Saboda waɗannan kalmomi fa, sai ɓaraka ta sāke shiga cikin Yahudawa. [20] Da
yawa daga cikinsu suka ce, "Yana da aljani, yana kuma hauka. Don me za ku saurare
shi?"

[21] Amma waɗansu suka ce, "Kai, waɗannan kalmomi ba na mai aljani ba ne. Anya,
aljani yana iya buɗe idanun makaho?"

### *Rashin bangaskiyar Yahudawa*

[22] Bikin Miƙawa* a Urushalima ya kewayo, lokacin sanyin hunturu ne kuwa. [23] Sai
ga Yesu a filin haikali yana zagawa a Shirayin Solomon, [24] sai Yahudawa suka taru
kewaye da shi, suka ce masa, "Har yaushe za ka bar mu da shakka? In kai ne Kiristin,
ka faɗa mana a fili mana."

[25] Yesu ya amsa ya ce, "Na faɗa muku, amma ba ku gaskata ba. Ayyukan da nake
yi cikin sunan Ubana su suke nuna ko wane ne ni. [26] Amma ba ku gaskata ba domin
ku ba tumakina ba ne. [27] Tumakina sukan saurari muryata; na sansu, suna kuma bi
na. [28] Ina ba su rai madawwami, ba za su taɓa hallaka ba; ba kuma mai ƙwace su
daga hannuna. [29] Ubana, wanda ya ba ni su, ya fi duka girma, ba mai ƙwace su daga
hannun Ubana. [30] Da ni da Uba ɗaya ne."

[31] Sai Yahudawa suka sāke ɗebo duwatsu don su jajjefe shi, [32] amma Yesu ya ce
musu, "Na nuna muku ayyukan alheri masu yawa da Uba ya aiko ni in yi, a kan
wanne kuke so ku jajjefe ni?"

[33] Yahudawa suka amsa suka ce, "Ai, ba don wani daga cikin waɗannan ayyukan
alheri ne muke so mu jajjefe ka ba, amma don saɓon da kake yi, kai da kake mutum
kawai, kana mai da kanka Allah."

[34] Yesu ya amsa musu ya ce, "Ba a rubuce yake a cikin Dokarku ba cewa, 'Na ce ku
alloli ne'†? [35] Mun dai san Nassi ba ya ƙarya, In har ya kira su waɗanda maganar
Allah ta zo musu, 'alloli,' [36] to, game da wanda Uba ya keɓe a matsayin nasa ne ya
kuma aiko shi duniya. Don me kuke ce saɓo nake, domin na ce, 'Ni Ɗan Allah ne?'
[37] In ba ayyukan da Ubana yake yi ne nake yi ba, to, kada ku gaskata ni. [38] Amma
in su nake yi, ko ba ku gaskata ni ba, to, ku gaskata ayyukan, don ku sani, ku kuma
gane, Uban yana cikina, ni kuma ina cikin Uban." [39] Sai suka sāke yin ƙoƙari su kama
shi, amma ya kuɓuce musu.

[40] Sa'an nan Yesu ya sāke koma ƙetaren Urdun inda dā Yohanna yake baftisma. A
can ya zauna [41] mutane da yawa suka zo wurinsa. Suka ce, "Ko da yake Yohanna bai
yi wani abin banmamaki ba, duk abubuwan da Yohanna ya faɗa game da mutumin
nan gaskiya ne." [42] A nan kuwa mutane da yawa suka gaskata da Yesu.

# 11

### *Mutuwar Lazarus*

[1] To, an yi wani mutum mai suna Lazarus wanda ya yi rashin lafiya. Shi daga
Betani ne, ƙauyen su Maryamu da 'yar'uwarta Marta. [2] Maryamun nan kuwa, wadda
ɗan'uwanta Lazarus yake rashin lafiya, ita ce ta zuba wa Ubangiji turare ta kuma
goge ƙafafunsa da gashin kanta. [3] Saboda haka 'yan'uwansa mata suka aika da saƙo
wa Yesu cewa, "Ubangiji, wannan da kake ƙauna yana rashin lafiya."

* **10:22** Wato, Hanukka † **10:34** Zab 82.6

4 Sa'ad da ya ji haka, sai Yesu ya ce, "Wannan rashin lafiya ba zai kai ga mutuwa
ba. A'a, sai dai don a ɗaukaka Allah a kuma ɗaukaka Ɗan Allah ta wurin wannan."
5 Yesu kuwa yana ƙaunar Marta da 'yar'uwarta da kuma Lazarus. 6 Duk da haka
sa'ad da ya ji Lazarus ba shi da lafiya, sai ya ƙara kwana biyu a inda yake.
7 Sai ya ce wa almajiransa, "Mu koma Yahudiya."
8 Sai suka ce, "Rabbi, ba da daɗewa ba ne Yahudawa suka nemi su jajjefe ka, duk
da haka za ka koma can?"
9 Yesu ya amsa ya ce, "Ba sa'a goma sha biyu ce yini guda ba? Mutumin da yake
tafiya da rana ba zai yi tuntuɓe ba gama yana ganin hasken duniyan nan. 10 Sai a
sa'ad da yake tafiya da dare ne zai yi tuntuɓe, don ba shi da haske."
11 Bayan ya faɗa haka, sai ya ƙara ce musu, "Abokinmu Lazarus ya yi barci, amma
za ni in tashe shi."
12 Almajiransa suka ce, "Ubangiji, in barci ne yake, to, ai, zai sami sauƙi." 13 Yesu
kuwa yana magana mutuwarsa ce, amma almajiransa suka ɗauka yana nufin barcin
gaskiya ne.
14 Saboda haka sai ya gaya musu a fili cewa, "Lazarus ya mutu, 15 amma saboda ku
na yi farin ciki da ba na can, domin ku gaskata. Amma mu dai je wurinsa."
16 Sai Toma (wanda ake kira Didaimus) ya ce wa sauran almajiran, "Mu ma mu je,
mu mutu tare da shi."

### *Yesu ya yi wa 'yan'uwan Lazarus mata ta'aziyya*

17 Da isowarsa, Yesu ya tarar Lazarus ya riga ya yi kwana huɗu a kabari. 18 Betani
bai kai mil biyu ba daga Urushalima, 19 Yahudawa da yawa kuwa suka zo wurin
Marta da Maryamu don su yi musu ta'aziyya, saboda rasuwar ɗan'uwansu. 20 Sa'ad
da Marta ta ji cewa Yesu yana zuwa, sai ta fita don ta tarye shi, amma Maryamu ta
zauna a gida.
21 Sai Marta ta ce wa Yesu, "Ubangiji, da kana nan da ɗan'uwana bai mutu ba.
22 Amma na san cewa ko yanzu ma Allah zai ba ka duk abin da ka roƙa."
23 Yesu ya ce mata, "Dan'uwanki zai sāke tashi."
24 Marta ta amsa ta ce, "Na sani zai sāke tashi a tashin matattu a rana ta ƙarshe."
25 Yesu ya ce mata, "Ni ne tashin matattu da kuma rai. Duk wanda ya gaskata da
ni zai rayu, ko ya mutu; 26 kuma duk wanda yake raye ya kuma gaskata da ni ba zai
taɓa mutuwa ba. Kin gaskata wannan?"
27 Sai ta ce masa, "I, Ubangiji, na gaskata kai ne Kiristi, Ɗan Allah, mai zuwa cikin
duniya."
28 Bayan ta faɗa haka kuwa, sai ta koma ta je ta kira 'yar'uwarta Maryamu a gefe.
Ta ce, "Ga Malam ya zo, kuma yana kiranki." 29 Sa'ad da Maryamu ta ji haka sai ta yi
wuf ta tafi wurinsa. 30 Yesu dai bai riga ya shiga ƙauyen ba tukuna, har yanzu yana
inda Marta ta tarye shi. 31 Da Yahudawan da suke tare da Maryamu a cikin gida, suke
mata ta'aziyya, suka ga ta yi wuf ta fita, sai suka bi ta, suna tsammani za tă kabarin
ne tă yi kuka a can.
32 Sa'ad da Maryamu ta kai inda Yesu yake, ta kuma gan shi, sai ta fāɗi a gabansa
ta ce, "Ubangiji, da kana nan, da ɗan'uwana bai mutu ba."
33 Da Yesu ya ga tana kuka, Yahudawan da suka zo tare da ita ma suna kuka, sai
ya yi juyayi ƙwarai a ruhu ya kuma damu. 34 Sai ya yi tambaya ya ce, "Ina kuka sa
shi?"
Suka amsa suka ce, "Ubangiji zo ka gani."
35 Yesu ya yi kuka.
36 Sai Yahudawa suka ce, "Dubi yadda yake ƙaunarsa!"
37 Amma waɗansunsu suka ce, "Anya, wanda ya buɗe wa makahon nan idanu, ba
zai iya yin wani abu yă hana wannan mutum mutuwa ba?"

### *Yesu ya tā da Lazarus daga matattu*

38 Yesu, har yanzu cike da juyayi, ya zo kabarin. Kogo ne da aka rufe bakin da
dutse. 39 Sai Yesu ya ce, "Ku kawar da dutsen."

Marta, 'yar'uwan mamacin ta ce, "Ubangiji, yanzu, ai, zai yi wari, don yau kwanansa huɗu ke nan a can."

40 Sai Yesu ya ce, "Ban gaya miki cewa in kin gaskata za ki ga ɗaukakar Allah ba?"

41 Saboda haka suka kawar da dutsen. Sa'an nan Yesu ya dubi sama ya ce, "Uba,
na gode maka da ka saurare ni. 42 Na san kullum kakan saurare ni, na dai faɗa haka
ne saboda amfanin mutanen nan da suke tsaitsaye, don su gaskata cewa kai ka aiko ni."

43 Sa'ad da ya faɗa haka, sai Yesu ya yi kira da babbar murya ya ce, "Lazarus, ka
fito!" 44 Sai mamacin ya fito, hannuwansa da ƙafafunsa a daure da ƙyallayen lilin,
fuskarsa kuwa an naɗe da mayafi.

Yesu ya ce musu, "Ku tuɓe kayan bizo, ku bar shi yă tafi."

### *An ƙulla shawara a kashe Yesu*
*(Mattiyu 26.1-5; Markus 14.1,2; Luka 22.1,2)*

45 Saboda haka Yahudawa da yawa da suka zo don su ziyarci Maryamu, suka kuma
ga abin da Yesu ya yi, suka ba da gaskiya gare shi. 46 Amma waɗansunsu suka je
wurin Farisiyawa suka gaya musu abin da Yesu ya yi. 47 Sai manyan firistoci da
Farisiyawa suka kira taron Majalisa.

Suka yi tambaya suna cewa, "Me muke yi ne? Ga mutumin nan yana yin abubuwan
banmamaki masu yawa. 48 In fa muka ƙyale shi ya ci gaba da haka, kowa zai gaskata
da shi, Romawa kuma su zo su karɓe wurinmu su kuma ƙwace ƙasarmu."

49 Sai waninsu, mai suna Kayifas, wanda ya kasance babban firist a shekarar ya
ce, "Ku dai ba ku san kome ba! 50 Ba ku gane ba, ai, gwamma mutum ɗaya yă mutu
saboda mutane da duk ƙasar ta hallaka."

51 Bai faɗa haka bisa nufinsa ba, sai dai a matsayinsa na babban firist a shekarar,
ya yi annabci ne cewa Yesu zai mutu saboda ƙasar Yahudawa, 52 ba don ƙasan nan
kaɗai ba amma don yă tattaro 'ya'yan Allah da suke warwatse ma, su zama ɗaya.
53 Saboda haka, daga wannan rana suka ƙulla su ɗauke ransa.

54 Saboda haka Yesu bai ƙara tafiya a cikin Yahudawa a sarari ba. A maimako haka sai ya janye zuwa yankin kusa da hamada, a wani ƙauye da ake kira Efraim, inda ya zauna da almajiransa.

55 Sa'ad da lokaci ya yi kusa a yi Bikin Ketarewa na Yahudawa, da yawa suka
haura daga ƙauyuka zuwa Urushalima, don su tsarkake kansu kafin Bikin Ketarewa.
56 Suka yi ta neman Yesu, da suke a tsaitsaye a filin haikali kuwa suka dinga tambayar
juna, suna cewa, "Me kuka gani? Anya, zai zo Bikin kuwa?" 57 Manyan firistoci da
Farisiyawa tuni sun riga sun yi umarni cewa duk wanda ya san inda Yesu yake, yă
faɗa don su kama shi.

## 12

### *An shafe Yesu da mai a Betani*
*(Mattiyu 26.6-13; Markus 14.3-9)*

1 Kwana shida kafin Bikin Ketarewa, sai Yesu ya iso Betani, inda Lazarus yake,
wanda Yesu ya tā da daga matattu. 2 A nan aka shirya abincin yamma don girmama
Yesu. Marta ta ce yi hidima, Lazarus kuma yana ɗaya cikin waɗanda suke ci tare shi.
3 Sai Maryamu ta ɗauki wajen awo guda na nardi zalla, turare mai tsada; ta zuba
a ƙafafun Yesu ta kuma goge ƙafafunsa da gashinta. Gidan duk ya cika da ƙanshin
turaren.

4 Amma ɗaya daga cikin almajiransa, Yahuda Iskariyot, wanda daga baya zai bashe
shi, bai amince ba ya ce, 5 “Don me ba a sayar da turaren nan aka kuma ba da kuɗin
ga matalauta ba? Ai, kuɗin ya kai albashin shekara guda.” 6 Ya yi wannan magana
ba don ya kula da matalauta ba ne, sai dai don shi ɓarawo ne. Da yake shi ne mai
ajiya jakar kuɗin, yakan taimaki kansa da abin da aka sa a ciki.

7 Yesu ya ce, “Ku ƙyale ta, an nufa ta ajiye wannan turaren don ranar jana’izata.
8 Kullum za ku kasance da matalauta, amma ba kullum za ku kasance tare da ni ba.”

9 Ana cikin haka sai babban taron Yahudawa suka sami labari Yesu yana can suka
kuwa zo, ba kawai don shi ba amma don su kuma ga Lazarus, wanda ya tā da daga
matattu. 10 Saboda haka manyan firistoci suka ƙulla su kashe Lazarus shi ma, 11 gama
dalilinsa Yahudawa da yawa suna komawa ga Yesu suna kuma ba da gaskiya gare
shi.

### *Shiga mai nasara*
### *(Mattiyu 21.1-11; Markus 11.1-11; Luka 19.28-40)*

12 Kashegari babban taron da suka zo Bikin suka sami labari cewa Yesu yana kan
hanyarsa zuwa Urushalima. 13 Sai suka ɗaɗɗauko rassan dabino suka fiffita taryensa,
suna ɗaga murya suna cewa,
“Hosanna!”

“Mai albarka ne wanda yake zuwa cikin sunan Ubangiji!”*

“Mai albarka ne Sarkin Isra’ila!”
14 Yesu ya sami ɗan jaki, ya hau, kamar yadda yake a rubuce cewa,
15 “Kada ki ji tsoro, ya Diyar Sihiyona;
duba, ga sarkinki yana zuwa,
zaune a kan aholaki jaki.”†

16 Da fari almajiransa ba su gane dukan wannan ba. Sai bayan da aka ɗaukaka
Yesu, sa’an nan suka gane cewa an rubuta waɗannan abubuwa game da shi ne, har
ma suka yi masa waɗannan abubuwa.

17 Taron da suke tare da shi a sa’ad da ya kira Lazarus daga kabari ya kuma tā da
shi daga matattu suka yi ta baza labarin. 18 Mutane da yawa kuwa suka fita taryensa,
saboda sun ji labarin abin banmamakin da ya yi. 19 Saboda haka Farisiyawa suka ce
wa juna, “Duba, wannan ba ya kai mu ko’ina. Ga shi, duk duniya tana bin sa!”

### *Yesu ya yi maganar mutuwarsa*

20 To, akwai waɗansu Hellenawa a cikin waɗanda suka haura don su yi sujada a
Bikin. 21 Suka zo wurin Filibus, wanda yake daga Betsaida ta Galili, da roƙo. Suka ce,
“Ranka yă daɗe, muna so mu ga Yesu.” 22 Sai Filibus ya je ya gaya wa Andarawus,
Andarawus da kuma Filibus suka gaya wa Yesu.

23 Yesu ya amsa ya ce, “Lokaci ya yi da za a ɗaukaka Ɗan Mutum. 24 Gaskiya nake
gaya muku, sai ƙwayar alkama ta fāɗi ƙasa ta mutu, in ba haka ba za tă kasance
ƙwaya ɗaya tak. Amma in ta mutu, za tă ba da ’ya’ya da yawa. 25 Duk mai ƙaunar
ransa, zai rasa shi, duk mai ƙin ransa a wannan duniya, zai kiyaye shi har yă zuwa
rai madawwami. 26 Duk wanda zai bauta mini dole yă bi ni, inda kuma nake, a can
bawana zai kasance. Ubana zai girmama wanda yake bauta mini.

27 “Yanzu kuwa na damu, amma me zan ce? ‘Uba, ka cece ni daga wannan sa’a’?
A’a, ai, saboda wannan dalili ne musamman na zo. 28 Uba, ka ɗaukaka sunanka!”

* **12:13** Zab 118.25,26 † **12:15** Zak 9.9

Sai wata murya ta fito daga sama ta ce, “Na riga na ɗaukaka shi, zan kuma ƙara
ɗaukaka shi.” 29 Taron da suke a wurin suka ji, suka ce an yi tsawa; waɗansu kuwa
suka ce mala’ika ne ya yi masa magana.

30 Yesu ya ce, “An yi wannan muryar saboda amfaninku ne, ba don nawa ba.
31 Yanzu ne za a yi wa duniyan nan shari’a, yanzu ne za a tumɓuke mai mulkin
duniyan nan. 32 Amma ni, sa’ad da aka ɗaga ni daga ƙasa, zan ja dukan mutane gare
ni.” 33 Ya faɗa haka ne don yǎ nuna irin mutuwar da zai yi.

34 Sai taron suka ce, “Ahab, Dokarmu ta gaya mana cewa, Kiristi zai kasance har
abada, to, yaya za ka ce, ‘Dole ne a ɗaga Ɗan Mutum?’ Wane ne wannan ‘Ɗan
Mutum’?”

35 Sai Yesu ya ce musu, “Haske zai kasance da ku na ɗan lokaci. Ku yi tafiya yayinda
hasken yana nan tare da ku, kada duhu yǎ cim muku. Mai tafiya a cikin duhu bai
san inda za shi ba. 36 Ku dogara ga hasken yayinda kuke da shi, don ku zama ’ya’yan
haske.” Da Yesu ya gama magana, sai ya tafi ya ɓuya daga gare su.

### *Yahudawa sun ci gaba da rashin bangaskiya*

37 Ko bayan Yesu ya yi dukan waɗannan abubuwan banmamaki a gabansu, duk
da haka ba su gaskata da shi ba. 38 Wannan ya faru ne, don a cika maganar annabi
Ishaya cewa,

“Ubangiji, wa ya gaskata saƙonmu,
ga wa kuma aka bayyana hannun ikon Ubangiji?”‡

39 Saboda haka ba su iya gaskatawa ba, domin, kamar yadda Ishaya ya faɗa a wani
wuri cewa,

40 “Ya makantar da idanunsu
ya kuma taurare zukatansu,
don kada su gani da idanunsu,
ko su fahimta a zukatansu,
ko kuwa su juyo, har in warkar da su.”§

41 Ishaya ya faɗi haka ne, saboda ya hangi ɗaukakar Yesu, ya kuwa yi magana a
kansa.

42 Duk da haka, da yawa har daga cikin shugabanni ma suka gaskata da shi. Amma
saboda Farisiyawa ba su furta bangaskiyarsu ba, don tsoron kada a kore su daga
majami’a; 43 gama sun fi son yabon mutane, fiye da yabon Allah.

44 Sa’an nan Yesu ya ɗaga murya ya ce, “Duk wanda ya gaskata da ni, ba ni yake
gaskatawa ba, amma ga wanda ya aiko ni ne. 45 Duk mai dubana, yana duban wanda
ya aiko ni ne. 46 Na zo cikin duniya a kan ni haske ne, don duk wanda ya gaskata da
ni, kada yǎ zauna a cikin duhu.

47 “Duk mai jin kalmomina bai kuwa kiyaye su ba, ba ni ba ne nake shari’anta shi.
Gama ban zo domin in yi wa duniya shari’a ba, sai dai domin in cece ta. 48 Akwai mai
hukunci saboda wanda ya ƙi ni, bai kuma karɓi kalmomina ba; wannan maganar da
na faɗa ita ce za tǎ hukunta shi a rana ta ƙarshe. 49 Gama ba don kaina na yi magana
ba, Uban da ya aiko ni shi kansa ne ya ba ni umarni a kan abin da zan faɗa da kuma
yadda zan faɗe shi. 50 Na san cewa umarninsa yana kai ga rai madawwami. Saboda
haka duk abin da na faɗa na faɗe shi ne kamar dai yadda Uba ya ce in faɗa.”

## 13

### *Yesu ya wanke kafafun almajiransa*

‡ **12:38** Ish 53.1 § **12:40** Ish 6.10

[1] Ana gab da Bikin Ketarewa. Yesu kuwa ya san cewa lokaci ya yi da zai bar
wannan duniya, yă koma wurin Uba. Da yake ya ƙaunaci waɗanda suke nasa a
duniya, yanzu kuwa ya nuna musu cikakkiyar ƙaunarsa.
[2] Ana cikin cin abincin yamma, Iblis kuwa ya riga ya zuga Yahuda Iskariyot, ɗan
Siman yă bashe Yesu. [3] Yesu kuwa ya san cewa, Uba ya sa dukan abubuwa a
ƙarƙashin ikonsa, ya kuma san cewa daga Allah ya zo, zai kuma koma wurin Allah;
[4] saboda haka ya tashi daga cin abincin, ya tuɓe rigarsa ta waje, ya ɗaura tawul a
ƙugunsa. [5] Bayan haka, sai ya zuba ruwa a cikin kwano, sa'an nan ya fara wanke
ƙafafun almajiransa, yana sharewa da tawul wanda ya ɗaura.
[6] Ya zo kan Siman Bitrus, wanda ya ce masa, "Ubangiji, kai za ka wanke ƙafafuna?"
[7] Yesu ya amsa ya ce, "Yanzu ba ka fahimci abin da nake yi ba, amma nan gaba za
ka gane."
[8] Sai Bitrus ya ce, "Faufau, ba za ka taɓa wanke ƙafafuna ba."
Yesu ya amsa ya ce, "Sai na wanke ka, in ba haka ba, ba ka da rabo a gare ni."
[9] Sai Siman Bitrus ya ce, "To, Ubangiji, ba ƙafafuna kaɗai ba har ma da hannuwana
da kaina kuma!"
[10] Yesu ya amsa ya ce, "Wanda ya riga ya yi wanka yana bukata yă wanke ƙafafunsa
ne kawai; dukan jikinsa yana da tsabta. Ku kuwa kuna da tsabta, ko da yake ba
kowannenku ba." [11] Gama ya san wanda zai bashe shi, shi ya sa ya ce, "Ba kowa ba
ne yake da tsabta."
[12] Da ya gama wanke ƙafafunsu, sai ya sa tufafinsa ya koma wurin zamansa. Ya
tambaye su ya ce, "Kun fahimci abin da na yi muku? [13] Kuna ce da ni 'Malam' da
kuma 'Ubangiji,' daidai ne kuwa, gama haka nake. [14] Da yake ni da nake Ubangijinku
da kuma Malaminku, na wanke ƙafafunku, haka ku ma ya kamata ku wanke ƙafafun
juna. [15] Na ba ku misali domin ku yi yadda na yi muku. [16] Gaskiya nake gaya muku,
ba bawan da ya fi maigidansa, ko ɗan saƙon da ya fi wanda ya aike shi. [17] Yanzu da
kuka san waɗannan abubuwa, ku masu albarka ne, in kuka yi su.

*Yesu ya yi maganar bashe shi*

[18] "Ba dukanku nake nufi ba; na san waɗanda na zaɓa. Wannan kuwa don a cika
Nassi ne da ya ce, 'Wanda ya ci burodina tare da ni ya tasar mini.'*
[19] "Ina faɗa muku yanzu tun kafin yă faru, domin in ya faru, ku gaskata cewa ni
ne Shi. [20] Gaskiya nake gaya muku, 'Duk wanda ya karɓi wani da na aiko, ni ne ya
karɓa ke nan. Kuma duk wanda ya karɓe ni, ya karɓi wanda ya aiko ni ne.' "

*(Mattiyu 26.20-25; Markus 14.17-21; Luka 22.21-23)*

[21] Bayan Yesu ya faɗi haka, sai ya yi juyayi a ruhu, ya kuma furta cewa, "Gaskiya
nake gaya muku, ɗayanku zai bashe ni."
[22] Almajiransa suka dubi juna, suka rasa ko da wa yake. [23] Ɗaya daga cikin
almajiran Yesu wanda yake ƙauna kuwa, yana zaune kusa da shi. [24] Sai Siman Bitrus
ya taɓa wannan almajirin ya ce, "Tambaye shi, wa yake nufi?"
[25] Shi kuwa da yake jingine kusa da Yesu, ya ce, "Ubangiji, wane ne?"
[26] Yesu ya amsa ya ce, "Shi ne wanda zan ba shi gutsurin burodin nan sa'ad da na
tsoma cikin kwanon." Da ya tsoma gutsurin burodin, sai ya ba wa Yahuda Iskariyot,
ɗan Siman. [27] Nan take bayan Yahuda ya karɓi burodin, sai Shaiɗan ya shige shi.
Sai Yesu ya ce masa, "Abin nan da kake niyyar yi, ka yi shi maza." [28] Amma ba
wani a wurin cin abincin da ya fahimci dalilin da ya sa Yesu ya faɗa masa haka. [29] Da
yake Yahuda ne ma'aji, waɗansunsu suka ɗauka Yesu yana ce masa yă sayi abin da
ake bukata don Bikin ne, ko kuwa yă ba wa matalauta wani abu. [30] Nan da nan da
Yahuda ya karɓi burodin, sai ya fita. A lokacin kuwa dare ya yi.

* **13:18** Zab 41.9

*Yesu ya yi zancen mūsun Bitrus*
31 Da ya tafi, sai Yesu ya ce, "Yanzu ne aka ɗaukaka Ɗan Mutum aka kuma ɗaukaka
Allah a cikinsa. 32 In kuwa Allah ya sami ɗaukaka a cikin Ɗan, Allah kuwa zai
ɗaukaka Ɗan zuwa ga zatinsa, zai kuma ɗaukaka shi nan take.
33 "'Ya'yana, zan kasance da ku na ɗan ƙanƙani lokaci ne. Za ku neme ni. Kuma
kamar yadda na gaya wa Yahudawa, haka nake gaya muku yanzu. Inda zan tafi, ba
za ku iya zuwa ba.
34 "Sabon umarni nake ba ku. Ku ƙaunaci juna. Kamar yadda na ƙaunace ku, ku
ma ku ƙaunaci juna. 35 Ta haka kowa zai san cewa ku almajiraina ne, in kuna ƙaunar
juna."
*(Mattiyu 26.31-35; Markus 14.27-31; Luka 22.31-34)*
36 Siman Bitrus ya tambaye shi ya ce, "Ubangiji ina za ka?"
Yesu ya amsa ya ce, "Wurin da za ni, ba za ka iya zuwa yanzu ba, amma za ka bi
ni daga baya."
37 Bitrus ya ce masa, "Ubangiji, don me ba zan binka yanzu ba? Zan ba da raina
saboda kai."
38 Sai Yesu ya amsa ya ce, "Anya, za ka iya ba da ranka saboda ni? Gaskiya nake
faɗa maka, kafin zakara yă yi cara, za ka yi mūsun sanina sau uku!

# 14

*Yesu ya ta'azantar da almajiransa*
1 "Kada zuciyarku ta ɓaci. Ku gaskata da Allah, ku kuma gaskata da ni. 2 A cikin
gidan Ubana akwai wurin zama da yawa; da a ce ba haka ba ne, da na gaya muku.
Za ni can don in shirya muku wuri. 3 In kuwa na tafi na shirya muku wuri, sai in
dawo in ɗauke ku ku kasance tare da ni don ku kasance inda nake. 4 Ai, kun san
hanyar zuwa inda za ni."

*Yesu shi ne hanyar zuwa gun Uba*
5 Sai Toma ya ce masa, "Ubangiji, ba mu san inda za ka ba, to, ta yaya za mu san
hanyar?"
6 Yesu ya amsa ya ce, "Ni ne hanya, ni ne gaskiya, ni ne kuma rai. Ba mai zuwa
wurin Uba sai dai ta wurina. 7 Da kun san ni, da za ku san Ubana ma. Daga yanzu,
kun san shi kun kuma gan shi."
8 Filibus ya ce, "Ubangiji, ka nuna mana Uban, wannan kuwa zai biya bukatarmu."
9 Yesu ya amsa ya ce, "Ba san ni ba, Filibus, duk da daɗewan nan da na yi tare
da ku? Duk wanda ya gan ni, ai, ya ga Uban. Yaya za ka ce, 'Ka nuna mana Uban'?
10 Ba ka gaskata cewa ina cikin Uba, Uba kuma yana cikina ba? Kalmomin da nake
gaya muku ba na kaina ba ne. Ai, Uban da yake raye a cikina ne yake aikinsa. 11 Ku
gaskata ni sa'ad da na ce ina cikin Uba, Uba kuma yana cikina. Ko kuwa ku gaskata
ni saboda ayyukan banmamakin su kansu. 12 Gaskiya nake gaya muku, duk wanda
yake da bangaskiya gare ni, zai yi abubuwan da ni nake yi. Zai ma yi abubuwa masu
girma fiye da waɗannan, don zan tafi wurin Uba. 13 Kuma zan yi duk abin da kuka
roƙa cikin sunana, don Ɗan ya kawo ɗaukaka ga Uban. 14 Za ku iya roƙe ni kome a
cikin sunana, zan kuwa yi.

*Yesu ya yi alkawarin Ruhu Mai Tsarki*
15 "In kuna ƙaunata za ku yi biyayya da umarnina. 16 Zan kuwa roƙi Uba, zai kuwa
ba ku wani Mai Taimakon da zai kasance tare da ku har abada, 17 Ruhun gaskiya.
Duniya ba ta iya karɓarsa, don ba ta ganinsa ba ta kuma san shi ba. Amma kun
san shi, saboda yana zama tare da ku zai kuma kasance a cikinku. 18 Ba zan bar ku
marayu ba; zan zo wurinku. 19 Ba da daɗewa ba, duniya ba za tă ƙara ganina ba,

amma za ku gan ni. Don ina raye, ku ma za ku rayu. [20] A ranan nan za ku sani
ina cikin Uba, ku kuma kuna cikina, ni kuma ina cikinku. [21] Duk wanda yake da
umarnaina yana kuma yin biyayya da su, shi ne wanda yake ƙaunata. Wanda yake
ƙaunata kuwa Ubana zai ƙaunace shi, ni ma zan ƙaunace shi, in kuma bayyana
kaina gare shi."
[22] Sai Yahuda (ba Yahuda Iskariyot ba) ya ce, "Ubangiji, me ya sa za ka bayyana
kanka gare mu amma ba ga duniya ba?"
[23] Yesu ya amsa ya ce, "Duk mai ƙaunata, zai yi biyayya da koyarwata. Ubana zai
ƙaunace shi, za mu kuwa zo wurinsa mu zauna tare da shi. [24] Wanda ba ya ƙaunata
ba zai yi biyayya da koyarwata ba. Waɗannan kalmomin da kuke ji ba nawa ba ne;
na Uba ne da ya aiko ni.
[25] "Duk wannan na faɗa ne yayinda ina tare da ku. [26] Amma Mai Taimako, Ruhu
Mai Tsarki, wanda Uba zai aiko cikin sunana, zai koya muku kome, zai kuma tuna
muku duk abin da na faɗa muku. [27] Salama na bari tare da ku; salamata nake ba ku.
Ba kamar yadda duniya take bayarwa nake ba ku ba. Kada zuciyarku ta ɓaci kada
kuma ku ji tsoro.
[28] "Kun dai ji na ce, 'Zan tafi in kuma sāke dawo wurinku.' In har kuna ƙaunata,
za ku yi farin ciki cewa za ni wurin Uba, domin kuwa Uban ya fi ni. [29] Na faɗa muku
tun kafin yă faru, domin in ya faru, ku gaskata. [30] Ba zan ƙara yi muku magana
ba, gama mai mulkin duniyan nan yana zuwa. Ba shi da iko a kaina, [31] amma dole
duniya ta koya cewa ina ƙaunar Uba, ina kuma yin yadda Ubana ya umarce ni.
"Ku zo, mu bar nan.

# 15

*Itacen inabi da kuma rassa*

[1] "Ni ne kuringar inabi na gaskiya, Ubana kuwa shi ne manomin. [2] Yakan sare
kowane reshe a cikina da ba ya 'ya'ya, amma yakan ƙundume kowane reshe da yake
ba da 'ya'ya, domin yă ƙara ba da 'ya'ya. [3] Kun riga kun zama masu tsabta saboda
maganar da na yi muku. [4] Ku kasance a cikina, ni kuma zan kasance a cikinku. Babu
reshen da zai iya yin 'ya'ya da kansa, dole yă kasance a jikin kuringar inabin. Haka
ku ma, ba za ku iya ba da 'ya'ya ba sai kun kasance a cikina.
[5] "Ni ne kuringar inabin; ku ne kuma rassan. In mutum ya kasance a cikina ni
kuma a cikinsa, zai ba da 'ya'ya da yawa; in ba tare da ni ba, ba za ku iya yin kome
ba. [6] Duk wanda bai kasance a cikina ba, yana kamar reshen da aka jefar yă bushe;
irin waɗannan rassan ne akan tattara, a jefa cikin wuta a ƙone. [7] In kun kasance a
cikina kalmomina kuma suka kasance a cikinku, ku roƙi kome da kuke so, za a kuwa
ba ku. [8] Wannan ne yakan kawo ɗaukaka ga Ubana, ku ba da 'ya'ya da yawa, kuna
kuma nuna kanku ku almajiraina ne.
[9] "Kamar yadda Uba ya ƙaunace ni, haka ni ma na ƙaunace ku. To, fa, ku
kasance cikin ƙaunata. [10] In kuka yi biyayya da umarnaina, za ku kasance a cikin
ƙaunata, kamar dai yadda na yi biyayya da umarnan Ubana na kuma kasance a
cikin ƙaunarsa. [11] Na gaya muku wannan domin murnata ta kasance a cikinku,
murnanku kuma ta zama cikakkiya. [12] Umarnina shi ne, Ku ƙaunaci juna kamar
yadda na ƙaunace ku. [13] Babu ƙaunar da ta fi wannan, a ce mutum ya ba da ransa
saboda abokansa. [14] Ku abokaina ne, in kun yi abin da na umarta. [15] Ba zan ƙara ce
da ku bayi ba, don bawa bai san abin da maigidansa yake yi ba. A maimako in ce da
ku abokai, domin na sanar da ku duk abin da na ji daga wurin Ubana. [16] Ba ku kuka
zaɓe ni ba, a'a, ni ne na zaɓe ku na kuma naɗa ku ku je ku ba da 'ya'ya-'ya'yan da za
su dawwama. Uba kuwa zai ba ku duk abin da kuka roƙa cikin sunana. [17] Umarnina
ke nan. Ku ƙaunaci juna.

### *Duniya ta ƙi jinin almajirai*

18 "In duniya ta ƙi ku, ku san cewa ta fara ƙin na ne. 19 Da ku na duniya ne, da ta
ƙaunaci abinta. Kamar yadda yake, ku ba na duniya ba ne, na zaɓe ku daga duniya,
shi ya sa duniya take ƙinku. 20 Ku tuna da kalmomin da na yi muku cewa, 'Ba bawan
da ya fi maigidansa,'*In sun tsananta mini, ku ma za su tsananta muku. Da sun yi
biyayya da koyarwata, da za su yi biyayya da taku ma. 21 Za su yi muku haka saboda
sunana, gama ba su san Wannan da ya aiko ni ba. 22 Da a ce ban zo na yi musu
magana ba, da ba su da zunubi. Yanzu kam, ba su da wata hujja a kan zunubinsu.
23 Wanda ya ƙi ni ya ƙi ya ƙi Ubana ma. 24 Da a ce ban yi ayyuka a cikinsu waɗanda
babu wani da ya taɓa yi ba, da ba su da zunubi. Amma yanzu sun ga waɗannan
ayyukan banmamaki, duk da haka sun ƙi ni sun kuma ƙi Ubana. 25 Amma wannan
ya faru ne domin a cika abin da yake a rubuce cikin Dokarsu cewa, 'Sun ƙi ni ba
dalili.'†

### *Aikin Ruhu Mai Tsarki*

26 "Sa'ad da Mai Taimako ya zo, wanda zan aiko muku daga wurin Uba, Ruhun
gaskiya wanda yake fitowa daga wurin Uba, zai ba da shaida game da ni. 27 Ku ma
dole ku ba da shaida, domin kun kasance tare da ni tun daga farko.

## 16

1 "Na faɗa muku wannan duka, domin kada ku bauɗe. 2 Za su kore ku daga
majami'a; lalle, lokaci yana zuwa da duk wanda ya kashe ku, zai ɗauka yana yin
wa Allah hidima ne. 3 Za su yi waɗannan abubuwa ne domin ba su san Uba ko ni ba.
4 Na faɗa muku wannan, domin in lokacin ya yi, ku tuna na gargaɗe ku. Ban faɗa
muku wannan tun da fari ba domin ina tare da ku.

### *Aikin Ruhu Mai Tsarki*

5 "Yanzu zan tafi wurin wanda ya aiko ni, duk da haka ba waninku da ya tambaye
ni, 'Ina za ka?' 6 Saboda na faɗa waɗannan abubuwa ga shi kun cika da baƙin ciki.
7 Amma gaskiya nake gaya muku. Don amfaninku ne zan tafi. Sai ko na tafi, in ba
haka ba Mai Taimakon nan ba zai zo muku ba. Amma in na tafi, zan aiko shi gare
ku. 8 Sa'ad da ya zo kuwa, zai kā da duniya a kan zunubi da adalci da kuma hukunci,
9 a kan zunubi, domin mutane ba su gaskata da ni ba; 10 a kan adalci, domin zan tafi
wurin Uba, inda ba za ku ƙara ganina ba; 11 a kan hukunci kuma, domin an yanke
hukunci a kan mai mulkin duniyan nan.
12 "Ina da sauran abubuwa da yawa da zan faɗa muku, amma ba za ku iya ɗauka
a yanzu ba. 13 Amma sa'ad da shi, Ruhun gaskiya ya zo, zai bi da ku zuwa ga dukan
gaskiya. Ba zai yi magana don kansa ba; zai faɗi abin da ya ji ne kaɗai, zai kuma
faɗa muku abin da bai faru ba tukuna. 14 Zai kawo ɗaukaka gare ni ta wurin ɗaukan
abin da yake nawa, ya bayyana muku. 15 Duk abin da yake na Uba nawa ne. Shi ya
sa na ce, 'Ruhun zai ɗauko daga abin da yake nawa, yă bayyana muku.' "

### *Baƙin cikin almajirai zai koma farin ciki*

16 Yesu ya ci gaba da cewa, "Jim kaɗan, ba za ku ƙara ganina ba, sa'an nan bayan
an jima kaɗan kuma, za ku gan ni."
17 A nan fa sai waɗansu almajiransa suka ce wa juna, "Me yake nufi da cewa, 'Jim
kaɗan ba za ku ƙara ganina ba, kuma bayan an jima kaɗan, za ku gan ni,' da kuma,
'Domin zan tafi wurin Uba'?" 18 Suka yi ta tambaya, "Me yake nufi da 'jim kaɗan'?
Ba mu fahimci abin da yake faɗi ba."
19 Yesu ya gane suna so su tambaye shi game da wannan, sai ya ce musu, "Kuna
tambayar juna game da abin da nake nufi da na ce, 'Jim kaɗan ba za ku ƙara ganina

---

* **15:20** Yoh 13.16 † **15:25** Zab 35.19; Zab 69.4

ba, da kuma bayan an jima kaɗan, za ku gan ni’? [20] Gaskiya nake gaya muku, za
ku yi kuka da kuma gunji, yayinda duniya take murna. Za ku yi baƙin ciki, amma
baƙin cikinku zai koma farin ciki. [21] Macen da za tă haihu takan yi naƙuda domin
lokacinta ya yi; amma sa’ad da ta haihu, sai ta manta da wahalar domin farin ciki
an haifi jariri a duniya. [22] Haka ku ma, yanzu ne lokacin baƙin cikinku, amma zan
sāke ganinku za ku kuma yi farin ciki, ba kuwa wanda zai ɗauke muku farin cikinku.
[23] A ranan nan, ba za ku sāke tambaya ta kome ba. Gaskiya nake gaya muku, Ubana
zai ba ku kome da kuka roƙa cikin sunana. [24] Har yanzu dai ba ku roƙi kome cikin
sunana ba. Ku roƙa za ku kuwa samu, farin cikinku kuwa zai zama cikakke.

[25] “Ko da yake ina magana da misalai, lokaci yana zuwa da ba zan ƙara yin magana
da misalai ba, sai dai in faɗa muku a fili game da Ubana. [26] A ranan nan, za ku roƙa
a cikin sunana. Ban ce zan roƙi Uba a madadinku ba. [27] Ai, shi Uban kansa yana
ƙaunarku domin kun ƙaunace ni kun kuma gaskata cewa daga Allah na fito. [28] Na
fito daga wurin Uba, na kuma shigo duniya, yanzu kuwa zan bar duniya in koma
wurin Uba.”

[29] Sai almajiran Yesu suka ce, “Haba, yanzu ne fa kake magana a sarari ba tare
da misalai ba. [30] Yanzu mun gane cewa ka san kome ba sai wani ya tambaye ka ba.
Wannan ya sa muka gaskata ka fito daga Allah.”

[31] Yesu ya amsa ya ce, “A ƙarshe kun gaskata! [32] Amma lokaci na zuwa, har ma ya
yi, da za a warwatsa ku, kowa yă koma gidansa. Za ku bar ni ni kaɗai. Duk da haka
ba ni kaɗai ba ne, gama Ubana yana tare da ni.

[33] “Na faɗa muku waɗannan abubuwa ne, domin a cikina ku sami salama. A
duniyan nan za ku sha wahala. Amma ku yi ƙarfin hali! Na yi nasara a kan duniya.”

# 17

### *Yesu ya yi addu’a*

[1] Bayan da Yesu ya faɗi wannan, sai ya dubi sama ya yi addu’a ya ce,

“Uba, lokaci ya yi. Ka ɗaukaka Ɗanka, don Ɗanka yă ɗaukaka ka. [2] Gama ka ba
shi iko bisa dukan mutane domin yă ba da rai madawwami ga duk waɗanda ka
ba shi. [3] Rai madawwami kuwa shi ne, su san ka, Allah makaɗaici mai gaskiya, da
kuma Yesu Kiristi, wanda ka aiko. [4] Na ɗaukaka ka a duniya ta wurin gama aikin
da ka ba ni. [5] Yanzu ya Uba, ka ɗaukaka ni a gabanka da ɗaukakar da dā nake da
ita tun kafin a kafa duniya.

### *Yesu ya yi addu’a saboda almajiransa*

[6] “Na bayyana ka ga waɗanda ka ba ni a duniya. Su naka ne; kai ka ba ni su
sun kuma yi biyayya da maganarka. [7] Yanzu sun san cewa duk abin da ka ba ni
daga gare ka ya fito. [8] Na ba su kalmomin da ka ba ni sun kuwa karɓa. Sun san
tabbatacce daga wurinka na fito. Sun kuma gaskata kai ka aiko ni. [9] Ina addu’a
dominsu. Ba domin duniya nake addu’a ba, amma domin waɗanda ka ba ni, gama
su naka ne. [10] Duk abin da nake da shi naka ne, kuma duk abin da kake da shi
nawa ne. Na kuwa sami ɗaukaka ta wurinsu. [11] Ba sauran zamana a duniya, amma
waɗannan a duniya suke, ni kuwa ina zuwa wurinka. Ya Uba Mai Tsarki, ka kiyaye
su ta wurin ikon sunanka, sunan da ka ba ni, don su zama ɗaya kamar yadda muke
ɗaya. [12] Yayinda nake tare da su, na kāre su na kuma kiyaye su ta wurin sunan
nan da ka ba ni. Ba ko ɗayan da ya ɓace, sai dai wannan da aka ƙaddara zuwa ga
hallaka don Nassi yă cika.

[13] “Yanzu ina zuwa wurinka, sai dai na faɗi waɗannan abubuwa ne tun ina a
duniya domin farin ciki yă zama cikakke a cikinsu. [14] Na gaya musu maganarka
duniya kuwa ta ƙi su, don su ba na duniya ba ne yadda ni ma ba na duniya ba ne.

15 Ba addu'ata ba ce ka ɗauke su daga duniya ba, sai dai ka kāre su daga mugun
nan. 16 Su ba na duniya ba ne, kamar yadda ni ma ba na duniya ba ne. 17 Ka
tsarkake su ta wurin gaskiya; maganarka ce gaskiya. 18 Kamar yadda ka aiko ni
cikin duniya, haka ni ma na aike su cikin duniya. 19 Saboda su ne na tsarkake
kaina, domin su ma a tsarkake su da gaske.

*Yesu ya yi addu'a saboda dukan masu bi*

20 "Addu'ata ba saboda masu bina kaɗai ba ne. Ina addu'a kuma saboda
waɗanda za su gaskata da ni ta wurin maganarsu. 21 Ina so dukansu su zama
ɗaya, ya Uba, kamar yadda kake a cikina, ni kuwa a cikinka. Haka su ma bari su
zauna cikinmu, domin duniya ta gaskata cewa kai ka aiko ni. 22 Na ba su ɗaukakar
da ka ba ni, don su zama ɗaya kamar yadda muke ɗaya. 23 Ni a cikinsu kai kuma
a cikina. Bari su kasance da cikakken haɗinkai, domin duniya ta san cewa kai ka
aiko ni. Ka kuwa ƙaunace su yadda ka ƙaunace ni.
24 "Uba, ina so waɗanda ka ba ni su kasance tare da ni a inda nake, su kuma ga
ɗaukakata, ɗaukakar da ka ba ni domin kana ƙaunata kafin halittar duniya.
25 "Ya Uba Mai Adalci, ko da yake duniya ba tă san ka ba, ni na san ka, sun kuma
san kai ka aiko ni. 26 Na bayyana ka a gare su, zan kuma ci gaba da bayyana ka
domin ƙaunar da ka yi mini ta kasance a cikinsu ni ma in kasance a cikinsu."

# 18

*An kama Yesu*
*(Mattiyu 26.47-56; Markus 14.43-50; Luka 22.47-53)*

1 Da ya gama addu'a, sai Yesu ya fita tare da almajiransa suka haye Kwarin Kidron.
A wancan ƙetaren kuwa akwai lambun zaitun, da shi da almajiransa suka shiga ciki.
2 To, Yahuda, wanda ya bashe shi, ya san wurin, domin Yesu ya sha zuwa wurin
da almajiransa. 3 Saboda haka Yahuda ya zo cikin lambun, yana jagoranta ƙungiyar
sojoji da waɗansu ma'aikata daga wurin manyan firistoci da Farisiyawa. Suna riƙe
da toci, fitilu da kuma makamai.
4 Yesu kuwa, sane da duk abin da zai same shi, ya fito ya tambaye, su ya ce, "Wa
kuke nema?"
5 Suka amsa suka ce, "Yesu Banazare."
Yesu ya ce, "Ni ne shi." (Yahuda kuwa wanda ya bashe shi yana nan tsaye tare da
su.) 6 Da Yesu ya ce, "Ni ne shi," sai suka ja da baya suka fāɗi a ƙasa.
7 Sai ya sāke tambayar su ya ce, "Wa kuke nema?"
Suka ce, "Yesu Banazare."
8 Yesu ya amsa ya ce, "Ai, na gaya muku ni ne shi. In kuma ni ne kuke nema, to,
sai ku bar waɗannan su tafi." 9 Wannan ya faru ne don a cika kalmomin da ya yi
cewa, "Ban yar da ko ɗaya daga cikin waɗanda ka ba ni ba."*
10 Sai Siman Bitrus, wanda yake da takobi, ya zāre, ya kai wa bawan babban firist
sara, ya ɗauke masa kunnensa na dama (Sunan bawan kuwa Malkus ne.)
11 Sai Yesu ya umarce Bitrus ya ce, "Mai da takobinka kube! Ba zan sha kwaf da
Uba ya ba ni ba?"

*An kai Yesu a gaban Annas*
*(Mattiyu 26.57,58; Markus 14.53,54; Luka 22.54)*

12 Sai ƙungiyar soja tare da shugaban sojanta da kuma ma'aikatan Yahudawa suka
kama Yesu. Suka daure shi 13 sa'an nan suka kawo shi da farko wurin Annas, wanda
yake surukin Kayifas, babban firist a shekaran nan. 14 Kayifas ne wanda ya shawarci
Yahudawa cewa zai fi kyau mutum ɗaya yă mutu saboda mutane.

* **18:9** Yoh 6.39

### *Mūsun Bitrus na farko*
### *(Mattiyu 26.69,70; Markus 14.66-68; Luka 22.55-57)*

15 Siman Bitrus da kuma wani almajiri suna bin Yesu. Domin almajirin nan sananne
ne ga babban firist, sai ya shiga tare da Yesu a filin gidan babban firist ɗin, 16 Bitrus
kuwa ya dakata a waje a bakin ƙofa. Almajirin nan da yake sananne ga babban firist,
ya dawo ya yi magana da yarinyar mai aiki a can, ya kuma shigo da Bitrus.
17 Yarinyar da take bakin ƙofar ta ce wa Bitrus, “Kai ba ɗaya ne daga cikin almajiran
mutumin nan ba ne?”
Bitrus ya amsa ya ce, “A'a, ba na ciki.”
18 To, ana sanyi, bayi da ma'aikatan suna tsattsaye kewaye da wutar da suka hura
don su ji ɗumi. Bitrus ma yana tsaye tare da su, yana jin ɗumi.

### *Babban firist ya yi wa Yesu tambayoyi*
### *(Mattiyu 26.59-66; Markus 14.55-64; Luka 22.66-71)*

19 Ana cikin haka, sai babban firist ya tuhumi Yesu game da almajiransa da kuma
koyarwarsa.
20 Yesu ya amsa ya ce, “Ai, na yi wa duniya magana a fili. Na kuma sha yin koyarwa
a majami'u ko kuma a haikali inda Yahudawa duka sukan taru. Ban taɓa faɗin kome
a ɓoye ba. 21 Don me kake tuhumata? Ka tambayi waɗanda suka ji ni. Ba shakka,
sun san abin da na faɗa.”
22 Da Yesu ya faɗa haka, sai ɗaya daga cikin ma'aikatan da yake tsaye kusa ya mare
shi a fuska ya ce, “Haka za ka amsa wa babban firist?”
23 Yesu ya amsa ya ce, “In na faɗi abin da ba daidai ba, ka nuna abin da ba daidai
ba. Amma in gaskiya na faɗa, don me ka mare ni?” 24 Sai Annas ya aika da shi, a
daure, wurin Kayifas babban firist.

### *Mūsun Bitrus na biyu da na uku*
### *(Mattiyu 26.71-75; Markus 14.69-72; Luka 22.58-62)*

25 Da Siman Bitrus yana nan tsaye yana jin ɗumin wuta, sai aka tambaye shi, “Kai,
kai ma ba ɗaya daga cikin almajiransa ba ne?”
Sai ya yi mūsu, yana cewa, “Sam, ba na ciki.”
26 Sai wani daga cikin bayin babban firist dangin wanda Bitrus ya sare wa kunne,
ya tambaya shi ya ce, “Kana tsammani ban gan ka tare da shi a gonar zaitun ba?”
27 Bitrus ya sāke yin mūsu, nan take kuwa zakara ya yi cara.

### *Yesu a gaban Bilatus*
### *(Mattiyu 27.1,2,11-14; Markus 15.1-5; Luka 23.1-5)*

28 Sa'an nan Yahudawa suka fitar da Yesu daga wurin Kayifas zuwa fadar gwamnar
Roma. A yanzu dai, safiya ta yi, don gudu kada su ƙazantar da kansu Yahudawa ba
su shiga cikin fadar ba; sun so su iya ci Bikin Ketarewa. 29 Saboda haka Bilatus ya
fito wajensu ya ce, “Wace ƙara kuke kawowa game da mutumin nan?”
30 Suka amsa suka ce, “Da a ce shi ba mai laifi ba ne, ai, da ba mu bashe shi gare
ka ba.”
31 Bilatus ya ce, “Ku tafi da shi da kanku mana, ku hukunta shi bisa ga dokarku.”
Sai Yahudawa suka ƙi suka ce, “Ba mu da ikon yanke wa wani hukuncin kisa.”
32 Wannan kuwa ya faru ne don a cika kalmomin da Yesu ya yi da suka nuna irin
mutuwar da zai yi.
33 Sai Bilatus ya koma cikin fada, ya kira Yesu ya tambaye shi, “Shin, kai ne sarkin
Yahudawa?”
34 Yesu ya yi tambaya ya ce, “Wannan ra'ayin kanka ne, ko waɗansu ne suka yi
maka magana game da ni?”

35 Bilatus ya amsa ya ce, “Ni mutumin Yahuda ne? Ai, mutanenka ne da kuma
manyan firistoci suka bashe ka gare ni. Me ka yi?”
36 Yesu ya ce, “Mulkina ba na duniyan nan ba ne. Da na duniyan nan ne da bayina
sun yi yaƙi su hana Yahudawa kama ni. Amma fa mulkina daga wani waje ne.”
37 Sai Bilatus ya ce, “To, wato, kai sarki ne!”
Yesu ya amsa ya ce, “Haka yake, ni sarki ne yadda ka faɗa. Tabbatacce, saboda
wannan dalili ne aka haife ni, kuma don wannan ne na zo duniya, domin in shaidi
gaskiya. Duk wanda yake gefen gaskiya yakan saurare ni.”
38 Bilatus ya tambaye shi ya ce, “Mece ce gaskiya?”

*(Mattiyu 27.15-31; Markus 15.6-20; Luka 23.13-25)*

Da ya faɗi haka, sai ya sāke fitowa wurin Yahudawa ya ce, “Ni fa ban sami wani
abin zargi game da shi ba. 39 Amma fa kuna da wata al’ada in lokacin Bikin Ketarewa
ya yi, nakan sakar muku da ɗan kurkuku ɗaya. To, kuna so in sakar muku ‘sarkin
Yahudawa’?”
40 Sai suka ɗau kururuwa suna cewa, “Kai, ba shi ba! A ba mu Barabbas!” To,
Barabbas ɗin nan yana da hannu dumu-dumu a wani tawaye.

# 19

*An yanke wa Yesu hukuncin mutuwar gicciye*

1 Sa’an nan Bilatus ya tafi da Yesu ya kuma sa aka yi masa bulala. 2 Sai sojojin suka
tuƙa rawanin ƙaya suka sa masa a kā, suka kuma yafa masa wata riga mai ruwan
shunayya. 3 Suka yi ta zuwa wurinsa suna cewa, “Ranka yă daɗe, sarkin Yahudawa!”
Suna ta marinsa a fuska.
4 Bilatus kuwa ya sāke fitowa ya ce wa Yahudawa, “Ga shi, zan fito muku da shi
don ku san cewa ban same shi da wani abin zargi ba.” 5 Sa’ad da Yesu ya fito sanye
da rawanin ƙayar da kuma riga mai ruwan shunayya, sai Bilatus ya ce musu, “Ga
mutumin!”
6 Nan da nan da manyan firistoci da ma’aikatansu suka gan shi, sai suka yi ihu
suka ce, “A gicciye! A gicciye!”
Amma Bilatus ya amsa ya ce, “Ku, ku ɗauke shi ku gicciye. Ni dai ban same shi da
wani abin zargi ba.”
7 Yahudawa dai suka nace suna cewa, “Mu fa muna da doka, kuma bisa ga dokar
dole yă mutu domin ya mai da kansa Ɗan Allah.”
8 Da Bilatus ya ji haka, sai tsoro ya ƙara kama shi, 9 sai ya sāke koma cikin fada.
Ya tambayi Yesu, “Daga ina ka fito?” Amma Yesu bai amsa masa ba. 10 Bilatus ya ce,
“Ba za ka yi mini magana ba? Ba ka san cewa ina da ikon sakinka, ko gicciye ka ba?”
11 Yesu ya amsa ya ce, “Ba ka da wani iko a kaina, in ba a ba ka daga sama ba.
Saboda haka wanda ya bashe ni gare ka, ya fi na zunubi.”
12 Daga nan fa, Bilatus ya yi nemi yă saki Yesu, sai dai Yahudawa suka yi ta ihu
suna cewa, “In ka saki wannan mutum, kai ba abokin Kaisar ba ne. Duk wanda ya
ɗauka kansa a matsayin sarki, ai, yana gāba da Kaisar ne.”
13 Da Bilatus ya ji haka, sai ya fito da Yesu, ya kuma zauna a kujerar shari’ar da ake
ce da shi Daɓen Dutse (wanda a harshen Arameyik ana ce da shi Gabbata). 14 Ranar
Shirye-shiryen Makon Bikin Ketarewa ce kuwa, wajen sa’a ta shida.
Sai Bilatus ya ce wa Yahudawa, “Ga sarkinku.”
15 Amma suka yi ihu suka ce, “A yi da shi! A yi da shi! A gicciye shi!”
Bilatus ya ce, “A! In gicciye sarkinku?”
Sai manyan firistoci suka amsa suka ce, “Mu dai, ba mu da wani sarki sai Kaisar.”
16 A ƙarshe Bilatus ya ba da shi gare su a gicciye shi.

### *Gicciyewa*
### *(Mattiyu 27.32-44; Markus 15.21-32; Luka 23.26-43)*

Saboda haka sojoji suka tafi da Yesu. 17 Ɗauke da gicciyensa, ya kuwa fita zuwa
wurin Koƙon Kai (wanda a harshen Arameya ana ce da shi Golgota). 18 Nan suka
gicciye shi tare da waɗansu mutum biyu, ɗaya a kowane gefe da Yesu a tsakiya.
19 Bilatus ya sa aka rubuta wata sanarwa aka kafa a kan gicciyen. Abin da aka
rubuta kuwa shi ne,

Yesu Banazare, Sarkin Yahudawa.

20 Yahudawa da yawa suka karanta wannan sanarwa, gama inda aka gicciye Yesu
yana kusa da birni. An kuwa rubuta sanarwar da Arameyanci, Romanci da kuma
Girik. 21 Sai manyan firistocin Yahudawa suka ce, “A’a! Kada ka rubuta, ‘Sarkin
Yahudawa,’ ka dai rubuta, wannan mutum ya ce shi sarkin Yahudawa ne.”
22 Bilatus ya amsa ya ce, “Abin da na rubuta, na rubuta.”
23 Da sojojin suka gicciye Yesu, sai suka ɗibi tufafinsa suka kasa kashi huɗu,
kowanne ya ɗauki kashi ɗaya. Suka kuma ɗauki taguwarsa, taguwar kuwa ba ɗinki,
saƙa ɗaya ce gudanta daga sama har ƙasa.
24 Sai suka ce wa juna, “Kada mu yage ta, sai dai mu jefa ƙuri’a a kanta mu ga
wanda zai ci.”

Wannan ya faru ne don a cika nassin da ya ce,

“Suka rarraba tufafina a junansu,
suka kuma jefa ƙuri’a a kan rigata.”[*]

Abin da sojojin suka yi ke nan.
25 To, tsaye kusa da gicciyen Yesu kuwa akwai mahaifiyarsa, tare da ’yar’uwar
mahaifiyarsa, Maryamu matar Kilofas, da kuma Maryamu Magdalin. 26 Sa’ad da Yesu
ya ga mahaifiyarsa a can, da kuma almajirin nan da yake ƙauna tsaye kusa, sai ya ce
wa mahaifiyarsa, “Mace, ga ɗanki,” 27 ga almajirin kuwa ya ce, “Ga mahaifiyarka.”
Tun daga wannan lokaci fa almajirin nan ya kai ta gidansa.

### *Mutuwar Yesu*
### *(Mattiyu 27.45-56; Markus 15.33-41; Luka 23.44-49)*

28 Bayan haka, sanin cewa an cika kome, kuma domin a cika Nassi, sai Yesu ya ce,
“Ina jin ƙishirwa.” 29 To, akwai wani tulun ruwan tsami ajiye a can, saboda haka
suka jiƙa soso da shi, suka soka soson a sandan itacen hizzob, suka kai bakin Yesu.
30 Da ya tsotsi abin sha ɗin, sai Yesu ya ce, “An gama.” Da wannan fa, ya sunkuyar
da kansa ya saki ruhunsa.
31 To, ranan nan fa, ranar Shirye-shirye ce, kashegari kuma muhimmin Asabbaci
ne. Domin Yahudawa ba sa so a bar jikunan a kan gicciyoyi a Asabbaci, sai suka roƙi
Bilatus a kakkarye ƙafafunsu kuma sauko da jikunan. 32 Sai sojoji suka zo suka karya
ƙafafun mutum na farko da aka gicciye tare da Yesu, da kuma na ɗayan. 33 Amma
sa’ad da suka zo kan Yesu suka tarar ya riga ya mutu, ba su karya ƙafafunsa ba.
34 A maimako, sai ɗaya daga cikin sojojin ya soki Yesu a gefe da māshi, nan take jini
da ruwa suka fito. 35 Mutumin da ya gani ɗin shi ya ba da shaida, shaidarsa kuwa
gaskiya ce. Ya san gaskiya yake faɗa, yana kuma ba da shaidar domin ku ma ku
gaskata. 36 Waɗannan abubuwa sun faru don a cika Nassi ne cewa, “Ba ko ɗaya daga
cikin ƙasusuwansa da za a karya,”[†] 37 kuma kamar yadda wani Nassi ya ce, “Za su
dubi wanda suka soka.”

### *Jana’izar Yesu*
### *(Mattiyu 27.57-61; Markus 15.42-47; Luka 23.50-56)*

---

[*] **19:24** Zab 22.18 [†] **19:36** Fit 12.46; Kid 9.12; Zab 34.20

38 Bayan haka, Yusuf mutumin Arimateya ya roƙi Bilatus a ba shi jikin Yesu. Yusuf
dai almajirin Yesu ne, amma a ɓoye domin yana tsoron Yahudawa. Da izinin Bilatus,
ya zo ya ɗauki jikin. 39 Yana tare da Nikodimus, wannan da ya taɓa zuwa wurin
Yesu da dare. Nikodimus ya zo da mur da aloyes a gauraye, wajen awo ɗari. 40 Da
ɗaukowar jikin Yesu, sai su biyun suka nannaɗe shi tare da kayan ƙanshi a cikin
ƙyallayen lilin bisa ga al'adar Yahudawa ta jana'iza. 41 A inda aka gicciye Yesu, akwai
wani lambu, a cikin lambun kuwa akwai sabon kabari, wanda ba a taɓa sa kowa ba.
42 Da yake ranan nan, ranar Shirye-shirye ce ta Yahudawa, kabarin kuma yana kusa,
sai suka binne Yesu a can.

# 20

### *Kabarin da ba kowa*
### *(Mattiyu 28.1-10; Markus 16.1-8; Luka 24.1-12)*

1 Da sassafe a ranar farko ta mako, tun da sauran duhu, Maryamu Magdalin ta tafi
kabarin ta kuwa tarar an kawar da dutsen daga bakin kabarin. 2 Sai ta zo da gudu
wajen Siman Bitrus da ɗayan almajirin, wanda Yesu yake ƙauna, ta ce, "Sun ɗauke
Ubangiji daga kabarin, ba mu kuma san inda suka sa shi ba!"
3 Sai Bitrus da almajirin nan suka nufi kabarin. 4 Dukansu biyu suna gudu, amma
ɗayan almajirin ya tsere wa Bitrus ya kuma fara kai kabarin. 5 Ya sunkuya ya duba
ciki ya ga ƙyallayen lilin ne kwance a can amma bai shiga ba. 6 Sa'an nan Siman
Bitrus, wanda yake bayansa, ya iso ya kuwa wuce cikin kabarin. Ya ga ƙyallayen
lilin kwance a can, 7 haka ma zanen binnewar da aka naɗe kan Yesu da shi. Zanen
a naɗe yake shi kaɗai, a keɓe da lilin ɗin. 8 A ƙarshe sai almajirin nan, wanda ya
kai kabarin da farko, shi ma ya shiga. Ya gani ya kuma gaskata. 9 (Har yanzu ba su
fahimci Nassin nan da ya ce lalle ne Yesu yǎ tashi daga matattu ba.) 10 Sai almajiran
suka koma zuwa inda suke zama.

### *Yesu ya bayyana ga Maryamu Magdalin*
### *(Mattiyu 28.1-10; Markus 16.1-8; Luka 24.1-12)*

11 Maryamu kuwa ta tsaya a bakin kabarin daga waje tana kuka. Da tana cikin
kuka, sai ta sunkuya ta leƙa cikin kabarin, 12 sai ta ga waɗansu mala'iku biyu saye
da fararen tufafi, zaune a inda dā gawar Yesu take, ɗaya wajen kai ɗayan kuma wajen
ƙafafu.
13 Suka tambaye ta cewa, "Mace, don me kike kuka?"
Ta ce, "Sun ɗauke Ubangijina, ban kuma san inda suka ajiye shi ba." 14 Da ta faɗin
haka, sai ta juya ta ga Yesu tsaye, sai dai ba tǎ gane cewa Yesu ne ba.
15 Sai ya ce, "Mace, don me kike kuka? Wa kike nema?"
Ta yi tsammani shi ne mai aikin lambun, sai ta ce, "Ranka yǎ daɗe, in kai ne ka
ɗauke shi, gaya mini inda ka ajiye shi, in je in ɗauke shi."
16 Yesu ya ce mata, "Maryamu."
Sai ta juya wajensa ta ɗaga murya ta ce da Arameyanci, "*Rabboni*!" (Wanda yake
nufin "Malam").
17 Yesu ya ce, "Kada ki riƙe ni, gama ban riga na koma wajen Uba tukuna ba.
A maimako, ki tafi wajen 'yan'uwana ki gaya musu, 'Ina komawa wajen Ubana da
Ubanku, wajen Allahna da kuma Allahnku.' "
18 Sai Maryamu Magdalin ta wajen almajiran da labari cewa, "Na ga Ubangiji!" Ta
kuma gaya musu cewa ya faɗa mata waɗannan abubuwa.

### *Yesu ya bayyana ga almajiransa*
### *(Mattiyu 28.16-20; Markus 16.14-18; Luka 24.36-49)*

19 Da Yamman ranar farko ta mako, sa'ad da almajiran suna tare, ƙofofi kuma suna
a kulle saboda tsoron Yahudawa, sai ga Yesu ya zo ya tsaya a tsakiyarsu ya ce, "Salama

tă kasance tare da ku!" [20] Bayan ya faɗa haka, sai ya nuna musu hannuwansa da
gefensa. Sai almajiran suka yi farin ciki ƙwarai da suka ga Ubangiji.
[21] Sai Yesu ya sāke ce musu, "Salama tă kasance tare da ku! Kamar yadda Uba ya
aiko ni, haka ni ma ina aikan ku." [22] Da wannan sai ya hura musu numfashinsa ya
ce, "Ku karɓi Ruhu Mai Tsarki. [23] Duk wanda kuka gafarta wa zunubansa, an gafarta
masa ke nan. Duk wanda ba ku gafarta wa ba kuwa, ba a gafarta masa ba ke nan."

*Yesu ya bayyana ga Toma*

[24] Toma kuwa (wanda ake kira Didaimus), ɗaya daga cikin Sha Biyun, ba ya tare da
almajiran sa'ad da Yesu ya zo. [25] Saboda haka sauran almajiran suka ce masa, "Ai,
mun ga Ubangiji!"
Amma ya ce musu, "Ina, ai, sai na ga ramin ƙusa a hannuwansa na sa yatsata a
inda ƙusoshi suka kasance, na kuma sa hannuna a gefensa, in ba haka ba, ba zan
gaskata ba."
[26] Bayan mako guda, har wa yau almajiransa suna cikin gidan, Toma kuwa yana
tare da su. Ko da yake ƙofofi suna kulle, sai ga Yesu ya zo ya tsaya a tsakiyarsu ya
ce, "Salama tă kasance tare da ku!" [27] Sa'an nan ya ce wa Toma, "Sa yatsarka nan;
dubi hannuwana. Miƙa hannunka ka sa a gefena. Ka daina shakka ka gaskata."
[28] Toma ya ce masa, "Ya Ubangijina da Allahna!"
[29] Sai Yesu ya ce masa, "Wato ka gaskata saboda ka gan ni ne, masu albarka ne
waɗanda ba su gan ni ba, amma suka gaskata."
[30] Yesu ya yi waɗansu abubuwan banmamaki da yawa a gaban almajiransa da ba
a rubuta a wannan littafi ba. [31] An dai rubuta waɗannan ne don ku gaskata Yesu ne
Kiristi, Ɗan Allah kuma ta wurin gaskatawa ku sami rai a cikin sunansa.

## 21

*Yesu da kamun kifin banmamaki*

[1] Daga baya Yesu ya sāke bayyana kansa ga almajiransa, a bakin Tekun Tibariya.*
Ga yadda ya faru. [2] Siman Bitrus, Toma (wanda ake kira Didaimus), Natanayel daga
Kana ta Galili, 'ya'yan Zebedi maza, da kuma waɗansu almajirai guda biyu suna tare.
[3] Sai Siman Bitrus ya ce musu, "Za ni kamun kifi," suka ce, "Za mu tafi tare da kai."
Saboda haka suka fita suka shiga jirgin ruwa, amma a daren nan ba su kama kome
ba.
[4] Da sassafe, sai ga Yesu tsaye a gaci, amma almajiran ba su gane cewa Yesu ne ba.
[5] Sai ya ce musu, "Abokai, kuna da kifi kuwa?"
Suka amsa suka ce, "A'a."
[6] Ya ce musu, "Ku jefa abin kamun kifinku dama da jirgin ruwan, za ku samu." Da
suka yi haka, sai suka kāsa jawo abin kamun kifin saboda yawan kifi.
[7] Sai almajirin da Yesu yake ƙauna ya ce wa Bitrus, "Ai, Ubangiji ne!" Nan da
nan da Siman Bitrus ya ji ya ce, "Ai, Ubangiji ne," sai ya yafa mayafinsa (don dā ma
ya tuɓe shi), ya fāɗa cikin ruwan. [8] Sauran almajiran kuwa suka bi shi cikin jirgin
ruwan, janye da abin kamun kifin cike da kifi, don ba su da nisa daga gaci, wajen
yadi ɗari ne. [9] Da suka sauka, sai suka ga garwashin wuta a can da kifi a kai, da
kuma 'yan burodi.
[10] Yesu ya ce musu, "Ku kawo waɗansu kifin da kuka kama yanzu." [11] Sai Siman
Bitrus ya hau ya jawo abin kamun kifin gaci. Ya cika da manyan kifi, 153, amma duk
da yawansun nan abin kamun kifin bai tsintsinke ba. [12] Yesu ya ce musu, "Ku zo
ku karya kumallo." Ba wani daga cikin almajiran da ya yi karambanin tambayarsa,
"Wane ne kai?" Sun san cewa Ubangiji ne. [13] Yesu ya zo, ya ɗauki burodin ya ba

* **21:1** Wato, Tekun Galili

su, haka kuma kifin. 14 Wannan fa shi ne sau na uku da Yesu ya bayyana kansa ga
almajiransa bayan an tashe shi daga matattu.

### *Yesu ya sāke tabbatar da Bitrus*

15 Da suka gama ci, sai Yesu ya ce wa Siman Bitrus, “Siman ɗan Yohanna, kana
ƙaunata da gaske fiye da waɗannan?”
Ya ce, “I, Ubangiji, ka san cewa ina sonka.”
Yesu ya ce, “Ciyar da ’ya’yan tumakina.”
16 Har wa yau Yesu ya ce, “Siman ɗan Yohanna, kana ƙaunata da gaske?”
Ya amsa ya ce, “I, Ubangiji, ka san cewa ina sonka.”
Yesu ya ce, “Lura da tumakina.”
17 Sau na uku ya ce masa, “Siman ɗan Yohanna, kana ƙaunata?”
Sai Bitrus ya ɓata rai saboda Yesu ya tambaye shi sau na uku, “Kana ƙaunata?” Ya
ce, “Ubangiji ka san kome duka; ka san cewa, ina ƙaunarka.”
Yesu ya ce, “Ciyar da tumakina. 18 Gaskiya nake faɗa maka, sa’ad da kake saurayi
kakan yi wa kanka sutura ka tafi inda ka so; amma sa’ad da ka tsufa za ka miƙa
hannuwanka, wani dabam yă yi maka sutura yă kai ka inda ba ka so.” 19 Yesu ya
faɗi wannan ne, don yă nuna irin mutuwar da Bitrus zai yi yă ɗaukaka Allah. Sa’an
nan ya ce masa, “Bi ni!”
20 Bitrus ya juya ya ga cewa almajirin nan da Yesu yake ƙauna yana binsu. (Wannan
ne ya jingina a jikin Yesu sa’ad da suke cin abincin yamman nan da ya ce, “Ubangiji
wane ne zai bashe ka?”) 21 Da Bitrus ya gan shi sai ya ce, “Ubangiji, wannan fa?”
22 Yesu ya amsa ya ce, “Idan na so yă kasance da rai har in dawo, mene ne naka a
ciki? Kai dai bi ni.” 23 Saboda wannan, jita-jita ta bazu a cikin ’yan’uwa cewa wannan
almajirin ba zai mutu ba. Amma fa Yesu bai ce ba zai mutu ba; shi dai ya ce, “In na
so yă kasance da rai har in dawo, mene ne naka a ciki?”
24 Wannan shi ne almajirin da ya ba da shaida a kan waɗannan abubuwa ya kuma
rubuta su. Mun san cewa shaidarsa gaskiya ce.
25 Yesu ya yi waɗansu abubuwa da yawa kuma. Da a ce an rubuta kowannensu,
na tabbata ko duniya duka ba za tă sami wuri saboda littattafan da za a rubuta ba.

# Ayyukan Manzanni

*An ɗauki Yesu zuwa sama*

1 A littafina na farko, Tiyofilus, na rubuta game da dukan abin da Yesu ya fara yi,
da abin da ya koyar 2 har zuwa ranar da aka ɗauke shi zuwa sama, bayan ya ba da
umarnai ta wurin Ruhu Mai Tsarki ga manzannin da ya zaɓa. 3 Bayan wahalarsa, ya
bayyana kansa ga waɗannan mutane ya kuma ba da tabbatattun alamu masu yawa
cewa yana da rai. Ya bayyana a gare su har kwana arbaʼin ya kuma yi musu magana
game da mulkin Allah. 4 A wani lokaci, yayinda yake ci tare da su, ya ba su wannan
umarni, "Kada ku bar Urushalima, amma ku jira kyautar da Ubana ya yi alkawari,
wadda kuka ji na yi magana a kai. 5 Gama Yohanna ya yi baftisma da[*]ruwa, amma
a cikin ʼyan kwanaki za a yi muku baftisma da Ruhu Mai Tsarki."
6 Saboda haka, saʼad da suka taru, sai suka tambaye shi, "Ubangiji, a wannan lokaci
za ka mayar da mulki ga Israʼila?"
7 Ya ce musu, "Ba naku ba ne ku san lokuta ko ranakun da Uban ya shirya cikin
ikonsa. 8 Amma ku za ku karɓi iko saʼad da Ruhu Mai Tsarki ya sauka a kanku; za ku
kuma zama shaiduna cikin Urushalima, da kuma cikin dukan Yahudiya da Samariya,
zuwa kuma iyakar duniya."
9 Bayan ya faɗi wannan, sai aka ɗauke shi sama a idanunsu sai wani girgije ya rufe
shi daga ganinsu.
10 Suna zuba ido a bisa, zuwa cikin sararin sama yayinda yake tafiya, nan da nan,
sai ga mutane biyu saye da fararen riguna tsaye kusa da su. 11 Sai suka ce, "Mutanen
Galili, don me kuke tsaye a nan kuna duban sararin sama? Wannan Yesu, wanda aka
ɗauke daga gare ku zuwa sama, zai komo daidai yadda kuka ga ya tafi sama."

*An zaɓi Mattiyas yă ɗauki matsayin Yahuda*

12 Sai suka koma Urushalima daga tudun da ake kira Dutsen Zaitun, tafiyar ranar
Asabbaci guda daga birnin. 13 Da suka iso, sai suka hau gidan sama, zuwa ɗakin da
suke zama. Waɗanda suka kasance kuwa su ne,

Bitrus, Yohanna, Yaƙub da Andarawus;
Filibus da Toma;
Bartolomeyu da Mattiyu;
Yaƙub ɗan Alfayus da Siman Zilot, da kuma Yahuda ɗan Yaƙub.

14 Waɗannan duka suka duƙufa cikin adduʼa, tare da waɗansu mata da Maryamu
mahaifiyar Yesu, da kuma tare da ʼyanʼuwansa.
15 A waɗancan kwanakin Bitrus ya miƙe tsaye cikin ʼyanʼuwa masu bi (taron da
ya yi kusan mutum ɗari da ashirin) 16 ya ce, "ʼYanʼuwana, dole a cika Nassin nan da
Ruhu Mai Tsarki ya yi magana tun da daɗewa ta bakin Dawuda game da Yahuda,
wanda ya zama jagora ga waɗanda suka kama Yesu 17 dā shi ɗaya ne cikinmu, ya
kuma yi hidima a cikin aikin nan."
18 (Da ladar da ya samu saboda muguntarsa Yahuda ya sayi wani fili; a can ya fāɗi
da kā, jikinsa ya fashe, hanjinsa kuma duk suka zubo. 19 Kowa a Urushalima ya ji
game da wannan, saboda haka suka kira wannan filin Akeldama, da yarensu, wato,
Filin Jini.)
20 Bitrus ya ce, "Gama yana a rubuce a cikin Littafin Zabura cewa,

[*] **1:5** Ko kuwa a cikin

" 'Bari wurinsa yă zama babu kowa;
kada kowa ya zauna a cikinsa,'†
kuma,
" 'Bari wani ya ɗauki matsayinsa na shugabanci.'‡
21 Saboda haka dole a zaɓi ɗaya daga cikin mutanen da suke tare da mu duk lokacin
da Ubangiji Yesu yake shiga da fita a cikinmu, 22 farawa daga baftisma ta Yohanna
har zuwa sa'ad da aka ɗauke Yesu daga gare mu. Gama dole ɗaya daga waɗannan
ya zama shaidar tashinsa daga matattu tare da mu."
23 Saboda haka suka gabatar da mutane biyu. Yusuf mai suna Barsabbas (da aka
kuma sani da Yustus) da kuma Mattiyas. 24 Sai suka yi addu'a suka ce, "Ubangiji, ka
san zuciyar kowa. Nuna mana wanne a cikin waɗannan biyu da ka zaɓa 25 ya karɓi
wannan aikin manzanci, wanda Yahuda ya bari don yă tafi wurin da yake nasa."
26 Sa'an nan suka jefa ƙuri'u, ƙuri'ar kuwa ta fāɗo a kan Mattiyas; sai aka sa shi
cikin manzannin nan goma sha ɗaya.

# 2

### *Ruhu Mai Tsarki ya zo a Fentekos*

1 Da ranar Fentekos ta yi, dukansu suna tare wuri ɗaya. 2 Ba zato ba tsammani sai
aka ji motsi kamar ta babbar iska tana hurowa daga sama ta kuma cika dukan gidan
da suke zaune. 3 Suka ga wani abin da ya yi kama da harsunan wuta, suka rarrabu
suna kuma sassauka a kan kowannensu. 4 Dukansu kuwa suka cika da Ruhu Mai
Tsarki suka kuma fara magana da waɗansu harsuna yadda Ruhu ya sa suka iya.
5 To, a Urushalima akwai Yahudawa masu tsoron Allah, daga kowace ƙasa a duniya.
6 Da suka ji wannan motsi, taro ya haɗu wuri ɗaya a ruɗe, domin kowannensu ya ji
suna magana da yarensa. 7 Cike da mamaki, suka yi tambaya suna cewa, "Ashe, duk
waɗannan mutane masu magana ba Galiliyawa ba ne? 8 To, yaya kowannenmu yana
ji suna yarensa? 9 Fartiyawa, Medes da Elamawa; mazaunan Mesofotamiya, Yahudiya
da Kaffadokiya, Fontus da Asiya, 10 Firjiya da Famfiliya, Masar da sassa Libiya kusa
da Sairin; baƙi daga Roma 11 (Yahudawa da kuma waɗanda suka tuba suka shiga
Yahudanci); Kiretawa da Larabawa, mun ji su suna shelar abubuwan banmamaki na
Allah da yarenmu!" 12 A ruɗe kuma cike da mamaki, suka tambayi junansu cewa,
"Mene ne wannan yake nufi?"
13 Duk da haka waɗansu suka yi musu ba'a suka ce, "Sun yi tatil da ruwan inabi
ne."

### *Bitrus ya yi wa taron jawabi*

14 Sai Bitrus ya miƙe tsaye tare da Sha Ɗayan nan, ya ɗaga muryarsa ya yi wa taron
jawabi ya ce, "'Yan'uwana Yahudawa da dukanku da kuke zama cikin Urushalima,
bari in bayyana muku wannan, ku saurara da kyau ga abin da zan faɗa. 15 Waɗannan
mutane ba su bugu ba, kamar yadda kuka ɗauka. Yanzu ƙarfe tara na safe ne kawai!
16 A'a, ai, abin da aka yi magana ta bakin annabi Yowel ke nan cewa,
17 "Allah ya ce, 'A kwanakin ƙarshe,
zan zubo Ruhuna bisa dukan mutane.
'Ya'yanku maza da mata za su yi annabci,
samarinku za su ga wahayoyi,
dattawanku kuma za su yi mafarkai.
18 Kai, har ma a kan bayina, maza da mata,
zan zubo Ruhuna a waɗancan kwanaki,
za su kuwa yi annabci.
19 Zan nuna abubuwan banmamaki a sararin sama

† **1:20** Zab 69.25 ‡ **1:20** Zab 109.8

da alamu a nan ƙasa,
jini da wuta da kuma hauhawan hayaƙi.
20 Za a mai da rana duhu,
wata kuma ya zama jini,
kafin zuwa rana mai girma da kuma ta ɗaukaka ta Ubangiji.
21 Kuma duk wanda ya kira
bisa sunan Ubangiji zai sami ceto.'*
22 "Mutanen Isra'ila, ku saurari wannan. Yesu Banazare shi ne mutumin da Allah ya
tabbatar muku ta wurin mu'ujizai, ayyukan banmamaki, da kuma alamu, waɗanda
Allah ya yi a cikinku ta wurinsa, kamar yadda ku kanku kuka sani. 23 An ba da
wannan mutum gare ku bisa ga nufin Allah da kuma rigyasaninsa, ku kuma tare da
taimakon mugayen mutane, kuka kashe shi ta wurin kafa shi a kan gicciye. 24 Amma
Allah ya tashe shi daga matattu, ya 'yantar da shi daga azabar mutuwa, don ba ya
yiwuwa mutuwa ta riƙe shi. 25 Dawuda ya yi faɗi game da shi cewa,
" 'Kullum ina ganin Ubangiji a gabana.
Gama yana a hannuna na dama,
ba zan jijjigu ba.
26 Saboda haka, zuciyata na farin ciki, harshena kuma na murna,
jikina kuma zai kasance da bege,
27 gama ba za ka bar ni cikin kabari ba,
ba kuwa za ka yarda Mai Tsarkinka yă ruɓa ba.
28 Ka sanar da ni hanyoyin rai,
za ka cika ni da farin ciki a gabanka.'†
29 "'Yan'uwa, zan iya tabbatar muku gabagadi cewa kakanmu Dawuda ya mutu
aka kuma binne shi, kabarinsa kuwa yana a nan har yă zuwa yau. 30 Amma shi
annabi ne ya kuma san abin da Allah ya yi masa alkawari da rantsuwa cewa zai
ɗora ɗaya daga cikin zuriyarsa a kan gadon sarautarsa. 31 Ganin abin da yake gaba,
ya yi magana a kan tashin Kiristi daga matattu cewa, ba a bar shi a kabari ba, jikinsa
kuma bai ruɓa ba. 32 Allah ya tashe wannan Yesu zuwa rai, mu kuwa duk shaidu ne
ga wannan. 33 An ɗaukaka shi zuwa ga hannun dama na Allah, ya karɓi alkawarin
Ruhu Mai Tsarki daga Uba, ya kuma zubo abin da yanzu kuke gani kuke kuma ji.
34 Gama Dawuda bai hau zuwa sama ba, duk da haka ya ce,
" 'Ubangiji ya ce wa Ubangijina,
"Zauna a hannun damana,
35 sai na sa abokan gābanka
su zama matashin sawunka." '‡
36 "Saboda haka bari dukan Isra'ila su tabbatar da wannan. Allah ya mai da
wannan Yesu, da kuka gicciye, Ubangiji da kuma Kiristi."
37 Sa'ad da mutane suka ji wannan, sai suka soku a zuci sai suka ce wa Bitrus da
sauran manzanni, "'Yan'uwa, me za mu yi?"
38 Bitrus ya amsa, "Ku tuba a kuma yi muku baftisma, kowannenku a cikin sunan
Yesu Kiristi domin gafarar zunubanku. Za ku kuwa karɓi kyautar Ruhu Mai Tsarki.
39 Alkawarin dominku ne da 'ya'yanku da kuma dukan waɗanda suke da nesa, domin
dukan waɗanda Ubangiji Allahnmu zai kira."
40 Da waɗansu kalmomi masu yawa ya gargaɗe su; ya kuma roƙe su cewa, "Ku ceci
kanku daga wannan lalataccen zamani." 41 Waɗanda suka yarda da saƙonsa kuwa
aka yi musu baftisma, a ranar kuwa yawansu ya ƙaru da mutum kusan dubu uku.

*Zumuncin masu bi*

* **2:21** Yow 2.28-32 † **2:28** Zab 16.8-11 ‡ **2:35** Zab 110.1

[42] Suka ba da kansu ga koyarwar manzanni da kuma ga zumunci, ga gutsuttsura
burodin da kuma ga addu'a. [43] Kowa ya cika da tsoro, manzannin kuwa suka aikata
abubuwan banmamaki da alamu masu yawa. [44] Dukan masu bi suna tare, suna
kuma mallakar kome tare. [45] Suka dinga sayar da ƙaddarorinsu da kayayyakinsu,
suka ba wa kowa gwargwadon bukatarsa. [46] Kowace rana suka ci gaba da taruwa a
filin haikali. Suka gutsuttsura burodi a gidajensu suna cin abinci tare da farin ciki
da zuciya ɗaya, [47] suna yabon Allah suna kuma samun tagomashin dukan mutane.
Ubangiji kuwa ya ƙara yawansu kowace rana na waɗanda suke samun ceto.

# 3

*Bitrus ya warkar da gurgu mai bara*

[1] Wata rana, Bitrus da Yohanna suna haurawa zuwa haikali a lokacin addu'a da
ƙarfe uku na rana. [2] To, sai ga wani da aka haifa gurgu ana ɗauke da shi zuwa ƙofar
haikalin da ake kira Kyakkyawa, inda akan ajiye kowace rana, don yǎ yi bara daga
masu shigowa cikin filayen haikali. [3] Da ya ga Bitrus da Yohanna suna gab da shiga,
sai ya roƙe su kuɗi. [4] Bitrus kuwa ya kafa masa ido, haka ma Yohanna. Sai Bitrus
ya ce, "Dube mu!" [5] Saboda haka mutumin ya mai da hankalinsa a kansu, yana fata
samun wani abu daga gare su.

[6] Sai Bitrus ya ce, "Azurfa ko zinariya ba ni da su, amma abin da nake da shi, shi zan
ba ka. A cikin sunan Yesu Kiristi Banazare, ka yi tafiya." [7] Ta wurin kama hannunsa
na dama, ya taimake shi ya miƙe, nan take ƙafafu da idon sawun mutumin suka yi
ƙarfi. [8] Sai ya yi wuf da ƙafafunsa ya fara tafiya. Ya tafi tare da su ya shiga cikin filin
haikali yana tafiya yana tsalle, yana kuma yabon Allah. [9] Sa'ad da dukan mutane
suka gan shi yana tafiya yana yabon Allah, [10] sai suka gane cewa shi ne mutumin
nan wanda dā yake zama yana bara a bakin ƙofar haikalin da ake kira Kyakkyawa,
suka kuwa cika da mamaki da tsoro a kan abin da ya faru gare shi.

*Bitrus ya yi wa masu kallo magana*

[11] Tun mai bawan yana riƙe da Bitrus da Yohanna, dukan mutanen suka yi mamaki,
suka zo wurinsu a guje a inda ake kira Shirayin Solomon. [12] Da Bitrus ya ga haka,
sai ya ce musu, "Mutanen Isra'ila, don me wannan ya ba ku mamaki? Don me kuke
kallonmu sai ka ce da ikon kanmu ne ko kuwa don ibadarmu ne muka sa wannan
mutum ya yi tafiya? [13] Allah na Ibrahim, Ishaku, da Yaƙub, Allah na kakanninmu, ya
ɗaukaka bawansa Yesu. Ku kuka ba da shi domin a kashe, kuka yi mūsun saninsa a
gaban Bilatus, ko da yake ya yi niyya ya sake shi. [14] Kuka yi mūsun sanin Mai Tsarki
da Mai Adalci kuka roƙa a sakar muku mai kisankai. [15] Kuka kashe tushen rai, amma
Allah ya tashe shi daga matattu. Mu shaidu ne ga wannan. [16] Ta wurin bangaskiya
cikin sunan Yesu ne wannan mutum da kuke gani kuka kuma sani ya sami ƙarfi. Da
sunan Yesu, da kuma bangaskiyar da take samuwa ta wurinsa ne ya ba shi cikakkiyar
warkarwa, yadda dukanku kuke gani.

[17] "To, 'yan'uwa, na san cewa, kun aikata wannan cikin jahilci ne, yadda
shugabanninku suka yi. [18] Amma ta haka ne Allah ya cika abin da ya rigyafaɗi
ta bakin dukan annabawa cewa, Kiristinsa zai sha wahala. [19] Saboda haka ku tuba,
ku juyo ga Allah, don a shafe zunubanku, don lokutan wartsakewa su zo daga wurin
Ubangiji, [20] don kuma ya iya aika da Kiristi, wanda aka naɗa tun dā saboda ku, Yesu
ke nan. [21] Dole yǎ kasance a sama, sai lokaci ya yi da Allah zai mai da kome sabo,
yadda ya yi alkawari tun dā ta wurin annabawansa masu tsarki. [22] Gama Musa ya
ce, 'Ubangiji Allahnku zai tasar muku wani annabi kamar ni daga cikin mutanenku;

dole ku saurari duk abin da ya faɗa muku. 23 Duk wanda bai saurare shi ba za a
ware shi gaba ɗaya daga mutanensa.'*
24 "Tabbatacce, dukan annabawa daga Sama'ila zuwa gaba, dukansu da suka yi
magana, sun rigya faɗin waɗannan kwanaki. 25 Ku kuwa magādan annabawan ne
da kuma na alkawarin da Allah ya yi da kakanninku. Ya ce wa Ibrahim, 'Ta wurin
zuriyarka, dukan kabilan duniya za su sami albarka.'† 26 Da Allah ya tashe bawansa,
ya aike shi da fari zuwa gare ku don yǎ albarkace ku ta wurin juye kowannenku daga
mugayen hanyoyinku."

# 4

*Bitrus da Yohanna a gaban majalisa*

1 Sai firistoci da shugaban masu gadin haikalin da kuma Sadukiyawa suka hauro
wurin Bitrus da Yohanna yayinda suke cikin magana da mutane. 2 Sun damu ƙwarai
da gaske domin manzannin suna koya wa mutane suna kuma shela a cikin Yesu cewa
akwai tashin matattu. 3 Sai suka kama Bitrus da Yohanna, amma da yake yamma ta
riga ta yi sai suka sa su cikin kurkuku sai kashegari. 4 Amma da yawa da suka ji
saƙon suka gaskata, yawan mutanen kuwa ya ƙaru ya kai wajen dubu biyar.
5 Kashegari, sai masu mulki, dattawa da kuma malaman dokoki suka taru a
Urushalima. 6 Annas babban firist yana nan, haka ma Kayifas Yohanna, Alekzanda
da kuma sauran mutanen da suke iyalin babban firist. 7 Suka sa aka kawo Bitrus da
Yohanna a gabansu suka kuma fara yin musu tambayoyi cewa, "Da wane iko ko da
wane suna kuka yi wannan?"
8 Sai Bitrus, cike da Ruhu Mai Tsarki ya ce musu, "Masu mulki da dattawan mutane!
9 In ana tuhumarmu ne yau saboda alherin da aka yi wa gurgun nan da kuma yadda
aka warkar da shi, 10 to, sai ku san wannan, ku da dukan mutanen Isra'ila cewa da
sunan Yesu Kiristi Banazare, wanda kuka gicciye amma wanda Allah ya tasar daga
matattu ne, wannan mutum yake tsaye a gabanku lafiyayye. 11 Shi ne,
" 'dutsen da ku magina kuka ƙi,
wanda kuwa ya zama dutsen kusurwar gini.'*
12 Ba a samun ceto ta wurin wani dabam, gama babu wani suna a ƙarƙashin sama
da aka ba wa mutane wanda ta wurinsa dole mu sami ceto."
13 Da suka ga ƙarfin halin Bitrus da Yohanna suka kuma gane cewa su marasa ilimi
ne, talakawa kuma, sai suka yi mamaki suka kuma lura cewa waɗannan mutane
sun kasance tare da Yesu. 14 Amma da yake sun ga mutumin da aka warkar yana
tsaye a wurin tare da su, sai suka rasa abin faɗi. 15 Saboda haka suka umarta a
fitar da su daga Majalisar, sa'an nan suka yi shawara da juna. 16 Suka ce, "Me za
mu yi da waɗannan mutane? Kowa da yake zama a Urushalima ya san sun yi abin
banmamaki, kuma ba za mu iya yin mūsu wannan ba. 17 Amma don a hana wannan
abu daga ƙara bazuwa cikin mutane, dole mu kwaɓe mutanen nan kada su ƙara yi
wa kowa magana cikin wannan suna."
18 Sai suka sāke kiransu ciki suka kuma umarce su kada su kuskura su yi magana
ko su ƙara koyarwa a cikin sunan Yesu. 19 Amma Bitrus da Yohanna suka amsa, "Ku
shari'anta da kanku ko daidai ne a gaban Allah mu yi muku biyayya maimakon Allah.
20 Gama ba za mu iya daina yin magana game da abin da muka gani muka kuma ji
ba."
21 Bayan ƙarin barazana sai suka bar su su tafi. Ba su iya yanke shawara yadda za a
hore su ba, domin dukan mutane suna yabon Allah saboda abin da ya faru. 22 Gama
mutumin da ya sami warkarwar banmamaki, shekarunsa sun fi arba'in.

* **3:23** M Sh 18.15,18,19 † **3:25** Far 22.18; Far 26.4 * **4:11** Zab 118.22

*Addu'ar masu bi*

23 Da aka sake su, Bitrus da Yohanna suka koma wajen mutanensu suka ba da
labarin duk abin da manyan firistoci da dattawa suka faɗa musu. 24 Sa'ad da suka
ji wannan, sai suka ɗaga muryoyinsu gaba ɗaya cikin addu'a ga Allah, suka ce, "Ya
Ubangiji Mai Iko Duka, kai ka halicci sama da ƙasa da kuma teku, da kome da yake
cikinsu. 25 Ka yi magana ta wurin Ruhu Mai Tsarki ta bakin bawanka, kakanmu
Dawuda cewa,

" 'Don me ƙasashe suke fushi,
mutane kuma suke ƙulla shawara a banza?
26 Sarakunan duniya sun ja dāgā,
masu mulki kuma sun taru gaba ɗaya,
suna gāba da Ubangiji
da kuma Shafaffensa†.'

27 Tabbatacce Hiridus da Buntus Bilatus suka haɗu tare da Al'ummai da kuma
mutanen Isra'ila a wannan birni ce don su ƙulla gāba da bawanka mai tsarki Yesu,
wanda ka shafe. 28 Sun aikata abin da ikonka da kuma nufinka ya riga ya shirya
tuntuni zai faru. 29 Yanzu, Ubangiji, ka dubi barazanansu ka kuma sa bayinka su
furta maganarka da iyakar ƙarfin hali. 30 Ka miƙa hannunka don ka warkar ka
kuma yi ayyukan banmamaki da alamu masu banmamaki ta wurin sunan bawanka
mai tsarki Yesu."

31 Bayan suka yi addu'a, sai inda suka taru ya jijjigu. Dukansu kuwa suka cika da
Ruhu Mai Tsarki, suka yi ta shaidar maganar Allah babu tsoro.

*Masu bi sun ba da mallakarsu a rarraba*

32 Dukan masu bi kuwa zuciyarsu ɗaya ne, nufinsu kuwa ɗaya. Babu wani da ya
ce abin da ya mallaka nasa ne, amma sun raba kome da suke da shi. 33 Da iko mai
ƙarfi manzanni suka ci gaba da shaidar tashin matattu na Ubangiji Yesu, alheri mai
yawa kuwa yana bisansu duka. 34 Babu mabukata a cikinsu. Lokaci-lokaci waɗanda
suke da gonaki ko gidaje sukan sayar da su, su kawo kuɗi daga abin da suka sayar,
35 su ajiye a sawun manzannin, a kuma raba wa kowa gwargwadon bukatarsa.

36 Yusuf, wani Balawe daga Saifurus, wanda manzanni suke kira Barnabas (wanda
yake nufin Ɗan Karfafawa) 37 ya sayar da wata gonar da ya mallaki ya kuma kawo
kuɗin ya ajiye a sawun manzanni.

# 5

*Ananiyas da Saffiratu*

1 To wani mutum mai suna Ananiyas tare da matarsa Saffiratu, shi ma ya sayar da
wata mallakarsa. 2 Da cikakken sanin matarsa ya ajiye sashi daga cikin kuɗin don
kansa, ya kuma kawo sauran ya ajiye a sawun manzanni.

3 Sai Bitrus ya ce, "Ananiyas, ta yaya Shaiɗan ya cika zuciyarka haka da ka yi wa
Ruhu Mai Tsarki ƙarya ka kuma ajiye wa kanka sauran kuɗin da ka karɓa na filin?
4 Ba naka ba ne kafin ka sayar da shi? Bayan da ka sayar da shi kuma, kuɗin ba naka
ba ne? Me ya sa ka yi tunanin yin irin wannan abu? Ba mutum ne ka yi wa ƙarya
ba, Allah ne ka yi masa."

5 Da Ananiyas ya ji wannan, sai ya fāɗi ya mutu. Sai babban tsoro kuwa ya kama
duk waɗanda suka ji abin da ya faru. 6 Sai samari suka zo gaba, suka naɗe gawarsa,
suka fitar da shi suka je suka binne.

7 Bayan kusan awa uku, sai matarsa ta shigo, ba da sanin abin da ya faru ba. 8 Bitrus
ya tambaye ta ya ce, "Gaya mini, kuɗin da yake da Ananiyas kuka sayar da filin ke
nan?"

Ta ce, "I, haka ne muka sayar."

† **4:26** Zab 2.1,2

9 Bitrus ya ce mata, “Ta yaya kuka yarda ku gwada Ruhun Ubangiji? Duba! Sawun
mutanen da suka binne mijinki suna bakin ƙofa, za su kuwa ɗauke ki zuwa waje ke
ma.”
10 Nan take ta fāɗi a ƙafafunsa ta mutu. Sai samarin suka shigo ciki, suka
kuwa same ta matacciya, suka ɗauke ta suka kai ta waje suka binne ta kusa da
mijinta. 11 Babban tsoro ya kama dukan ikkilisiya da kuma duk wanda ya ji game da
abubuwan nan.

*Manzanni sun warkar da mutane da yawa*

12 Manzannin suka yi ayyukan da alamu masu banmamaki masu yawa a cikin
mutanen. Dukan masu bi kuwa sukan taru a Shirayin Solomon. 13 Ba wanda ya yi
karambanin shiga cikinsu, duk da haka mutane suna girmama su ƙwarai. 14 Duk
da haka, maza da matan da suke gaskata ga Ubangiji sai ƙaruwa suke, suka kuma
ƙaru a yawa. 15 A sakamakon haka, mutane suka kawo marasa lafiya a tituna suka
kwantar da su a kan gadaje da tabarmai domin aƙalla inuwar Bitrus za tă bi kan
waɗansunsu yayinda yake wucewa. 16 Jama’a ma suka tattaru daga garuruwa kewaye
da Urushalima suna kawo marasa lafiyarsu da kuma waɗanda mugayen ruhohi suke
damun su, dukansu kuwa suka warke.

*An tsananta wa manzanni*

17 Sai babban firist da dukan abokan aikinsa, waɗanda suke na ƙungiyar
Sadukiyawa suka cika da kishi. 18 Suka kama manzannin suka sa su a kurkukun
da ake sa kowa da kowa. 19 Amma da dare wani mala’ikan Ubangiji ya buɗe ƙofofin
kurkukun ya fitar da su. 20 Ya ce, “Ku je ku tsaya a filin haikali ku sanar wa mutane
cikakken saƙon wannan sabon rai.”
21 Da gari ya waye, sai suka shiga filin haikali, yadda aka faɗa musu, suka kuwa
fara koyar da mutane.
Sa’ad da babban firist da abokan aikinsa suka iso, sai suka kira Majalisa gaba ɗaya
dukan dattawan Isra’ila, suka kuma aika kurkuku a zo da manzannin. 22 Amma da
dogarawan suka iso kurkukun, ba su same su a can ba. Saboda haka suka dawo
suka ba da labari, suka ce, 23 “Mun iske kurkukun a kulle sosai, da masu gadi suna
tsaye a bakin ƙofofin; amma da muka buɗe su, sai muka tarar ba kowa a ciki.” 24 Da
jin wannan labari, sai shugaban masu gadin haikali da manyan firistocin suka ruɗe,
suna tunanin abin da wannan al’amari zai zama.
25 Sai wani ya zo ya ce, “Ga shi! Mutanen da kuka sa a kurkuku suna tsaye a filin
haikali suna koya wa mutane.” 26 Da wannan, shugaban ya tafi tare da dogarawansa
suka kawo manzannin. Sun kawo su amma fa ba ƙarfi da yaji ba, don suna tsoro
kada mutane su jajjefe su da duwatsu.
27 Da suka kawo manzannin, sai suka sa su suka bayyana a gaban Majalisar don
babban firist ya tuhume su. 28 Ya ce, “Mun kwaɓe ku da gaske kada ku ƙara koyarwa
cikin wannan suna, duk da haka kun cika Urushalima da koyarwarku, har ma kuna
so ku ɗora mana laifin jinin mutumin nan.”
29 Bitrus da sauran manzannin suka amsa suka ce, “Dole ne mu yi wa Allah biyayya
a maimakon mutane! 30 Allahn kakanninmu ya tā da Yesu daga matattu, wanda kuka
kashe ta wurin ratayewa a bisan itace. 31 Allah ya ɗaukaka shi zuwa hannun damansa
a matsayin Yerima da Mai Ceto don yă kawo tuba da gafarar zunubai ga Isra’ila. 32 Mu
shaidu ne ga waɗannan abubuwa, haka kuma Ruhu Mai Tsarki, wanda Allah ya ba
wa waɗanda suke yin masa biyayya.”
33 Da suka ji haka, sai suka yi fushi suka so su kashe su. 34 Amma wani Bafarisiyen
da ake kira Gamaliyel, wani malamin doka, wanda dukan mutane ke girmamawa, ya
miƙe tsaye a Majalisar ya umarta a fitar da mutanen waje na ɗan lokaci. 35 Sa’an
nan ya yi musu jawabi ya ce, “Mutanen Isra’ila, ku yi kula da kyau da abin da kuke

niyyar yi wa mutanen nan. 36 Kwanan baya, Teyudas ya ɓullo, yana cewa wai shi
wani mutum ne, kuma wajen mutane ɗari huɗu suka bi shi. Aka kuwa kashe shi,
dukan masu binsa kuwa suka watse, kome ya wargaje. 37 Bayansa, Yahuda mutumin
Galili ya ɓullo a kwanakin ƙidaya, ya jagoranci mutane cikin tawaye. Shi ma aka
kashe shi, dukan mabiyansa kuma aka watsar da su. 38 Saboda haka, a wannan batu
na yanzu, ina ba ku shawara. Ku ƙyale mutanen nan! Ku bar su su tafi! Gama in
manufarsu ko ayyukansu na mutum ne, ai, zai rushe. 39 Amma in daga Allah ne, ba
za ku iya hana waɗannan mutane ba, za ku dai sami kanku kuna gāba da Allah ne."
40 Jawabinsa ya rinjaye su. Suka kira manzannin suka sa aka yi musu bulala. Sa'an
nan suka kwaɓe su kada su ƙara magana a cikin sunan Yesu, suka kuma bar su suka
tafi.
41 Manzannin suka bar Majalisar, suna farin ciki domin an ga sun cancanta a
kunyata su saboda Sunan nan. 42 Kowace rana, a filin haikali da kuma gida-gida,
ba su fasa koyarwa da kuma shelar labari mai daɗi cewa Yesu shi ne Kiristi ba.

# 6

*Zaɓen mutane bakwai*

1 A waɗannan kwanaki, sa'ad da yawan almajirai suke ƙaruwa, sai Yahudawan
masu jin Hellenanci a cikinsu suka yi gunaguni a kan Yahudawan da suke Ibraniyawa
domin ba a kula da gwaurayensu a wajen raba abinci na yau da kullum. 2 Saboda
haka Sha Biyun nan suka tara dukan almajirai wuri ɗaya, suka ce, "Bai zai yi kyau
mu bar hidimar maganar Allah don mu shiga hidimar abinci ba. 3 'Yan'uwa, ku zaɓi
mutum bakwai daga cikinku waɗanda aka sani suna cike da Ruhu da kuma hikima.
Mu kuwa za mu danƙa musu wannan aiki 4 mu kuwa mu mai da halinmu ga yin
addu'a da kuma hidimar maganar Allah."
5 Wannan shawarar kuwa ta gamshi dukan ƙungiyar. Sai suka zaɓi Istifanus,
mutumin da yake cike da bangaskiya da kuma Ruhu Mai Tsarki; da Filibus,
Burokorus, Nikano, Timon, Farmenas, da Nikolas daga Antiyok, wanda ya tuba zuwa
Yahudanci. 6 Suka gabatar da waɗannan mutane wa manzanni, waɗanda kuwa suka
yi addu'a, suka ɗibiya hannuwansu a kansu.
7 Saboda haka maganar Allah ta yaɗu. Yawan almajirai a Urushalima kuwa ya
yi saurin ƙaruwa, firistoci masu yawa kuma suka zama masu biyayya ga wannan
bangaskiya.

*An kama Istifanus*

8 To, Istifanus, mutum cike da alheri da ikon Allah, ya aikata manyan ayyukan
da alamu masu banmamaki a cikin mutane. 9 Sai hamayya ta taso daga 'yan
ƙungiyar Majami'a na 'Yantattu (kamar yadda ake kiransu), Yahudawan Sairin
da Alekzandariya da kuma lardunan Silisiya da Asiya. Mutanen nan suka fara
muhawwara da Istifanus, 10 amma ba su iya cin nasara kan hikimarsa ko kuma a
kan Ruhu wanda ta wurinsa ne ya magana ba.
11 Sa'an nan a asirce suka zuga waɗansu mutane su ce, "Mun ji Istifanus ya faɗa
kalmomin saɓo game da Musa da kuma Allah."
12 Ta haka suka tā da hankalin mutane da dattawa da kuma malaman dokoki. Suka
kama Istifanus suka kawo shi a gaban Majalisa. 13 Suka kawo masu ba da shaidar
ƙarya, waɗanda suka ba da shaida cewa, "Wannan mutum ba ya rabuwa da maganar
banza a kan wurin nan mai tsarki da kuma doka. 14 Gama mun ji shi yana cewa
wannan Yesu Banazare zai rushe wurin nan ya kuma canja al'adun da Musa ya ba
mu."
15 Dukan waɗanda suke zaune a Majalisar suka kafa wa Istifanus ido, suka kuma
ga fuskarsa ta yi kama da ta mala'ika.

# 7

*Jawabin Istifanus ga majalisa*

1 Sai babban firist ya tambaye shi ya ce, "Waɗannan zargen gaskiya ne?"

2 Game da wannan ya amsa ya ce, "'Yan'uwa da ubanni, ku saurare ni! Allah
mai ɗaukaka ya bayyana ga kakanmu Ibrahim yayinda yake a ƙasar Mesofotamiya
tukuna, kafin ya yi zama a Haran. 3 Allah ya ce, 'Ka bar ƙasarka da kuma mutanenka,
ka tafi ƙasar da zan nuna maka.'*

4 "Saboda haka ya bar ƙasar Kaldiyawa ya kuma yi zama a Haran. Bayan mutuwar
mahaifinsa, Allah ya aika da shi wannan ƙasar da yanzu kuke zama. 5 Bai ba shi
gādo a nan ba, ko taki ɗaya na ƙasa. Amma Allah ya yi masa alkawari cewa shi da
zuriyarsa masu zuwa bayansa za su mallaki ƙasar, ko da yake a lokacin Ibrahim ba
shi da yaro. 6 Allah ya yi magana da shi ta haka, 'Shekara ɗari huɗu, zuriyarka za
tă yi baƙunci a wata ƙasar da ba tasu ba, za su yi bauta su kuma sha wulaƙanci.
7 Amma zan hore ƙasar da suka bauta wa.' Allah ya ce, 'Kuma daga baya za su
fita daga wannan ƙasa su kuma yi mini sujada a wannan wuri.'† 8 Sa'an nan ya yi
wa Ibrahim alkawari game da kaciya. Ibrahim kuwa ya zama mahaifin Ishaku ya
kuma yi masa kaciya kwana takwas bayan haihuwarsa. Daga baya Ishaku ya zama
mahaifin Yaƙub, Yaƙub kuma ya zama mahaifin kakanninmu sha biyun nan.

9 "Domin kakanninmu sun ji kishin Yusuf, sai suka sayar da shi bawa zuwa Masar.
Amma Allah ya kasance tare da shi 10 ya kuma cece shi daga dukan wahalolinsa. Ya
ba wa Yusuf hikima ya kuma sa ya sami farin jini a wurin Fir'auna, sarkin Masar;
saboda haka ya mai da shi mai mulki a kan Masar da kuma dukan fadarsa.

11 "Sai yunwa ta auko wa dukan Masar da Kan'ana, ta kawo wahala mai tsanani,
kakanninmu ba su iya samun abinci ba. 12 Sa'ad da Yaƙub ya ji cewa akwai hatsi
a Masar, sai ya aiki kakanninmu ziyararsu ta farko. 13 A ziyararsu ta biyu, Yusuf
ya faɗa wa 'yan'uwansa wane ne shi, Fir'auna kuwa ya sami sani game da iyalin
Yusuf. 14 Bayan wannan, Yusuf ya aika a zo da mahaifinsa Yaƙub da dukan iyalinsa,
gaba ɗaya dai mutum saba'in da biyar ne. 15 Sai Yaƙub ya gangara zuwa Masar, inda
shi da kuma kakanninmu suka mutu. 16 Aka dawo da gawawwakinsu Shekem aka
binne su a kabarin da Ibrahim ya saya daga wurin 'ya'yan Hamor da waɗansu kuɗi
a Shekem.

17 "Da lokaci ya yi kusa da Allah zai cika alkawarin da ya yi wa Ibrahim, sai yawan
mutanenmu da suke a Masar ya ƙaru ƙwarai. 18 Sa'an nan wani sarki, wanda bai
san kome game da Yusuf ba, ya zama mai mulkin Masar. 19 Ya kuwa wulaƙanta
mutanenmu sosai, ya kuma gwada wa kakanni-kakanninmu azaba ta wurin tilasta
su su zubar da sababbin jariransu, don su mutu.

20 "A lokacin nan aka haifi Musa, shi kuwa ba kamar sauran jarirai ba ne. Wata uku
aka yi renonsa a gidan mahaifinsa. 21 Sa'ad da aka ajiye shi a waje, diyar Fir'auna ta
ɗauke shi ta kuma rene shi kamar ɗanta. 22 Musa ya sami ilimi cikin dukan hikimar
Masarawa ya kuma zama mai iko cikin magana da ayyuka.

23 "Da Musa ya cika shekara arba'in da haihuwa, sai ya yanke shawara yă ziyarci
'yan'uwansa Isra'ilawa. 24 Ya ga ɗayansu yana shan wulaƙanci a hannun wani
mutumin Masar, sai ya je ya kāre shi, ya rama masa ta wurin kashe mutumin Masar
ɗin. 25 Musa ya yi tsammani mutanensa za su gane cewa, Allah yana amfani da shi
don yă cece su, amma ba su gane ba. 26 Kashegari, Musa ya sadu da Isra'ilawa biyu
suna faɗa. Ya yi ƙoƙari ya sasanta su, yana cewa, 'Ku mutane, ku 'yan'uwa ne, don
me kuke so ku cutar da juna?'

* **7:3** Far 12.1 † **7:7** Far 15.13,14

27 “Amma mutumin da yake wulaƙanta ɗayan, ya tura Musa a gefe ya ce, ‘Wa ya
mai da kai mai mulki, da alƙali a kanmu? 28 Kana so ka kashe ni kamar yadda ka
kashe mutumin Masar nan na jiya?’‡ 29 Sa’ad da Musa ya ji haka, sai ya gudu zuwa
ƙasar Midiyan, inda ya yi baƙunci, ya kuma haifi ’ya’ya biyu maza.

30 “Bayan shekaru arba’in suka wuce, sai mala’ika ya bayyana ga Musa cikin
harshen wuta a ɗan itace a hamada kusa da Dutsen Sinai. 31 Sa’ad da ya ga haka,
ya yi mamakin abin da ya gani. Da ya yi kusa domin ya duba sosai, sai ya ji muryar
Ubangiji ta ce, 32 ‘Ni ne Allahn kakanninka, Allah na Ibrahim, Ishaku, da kuma
Yaƙub.’§ Sai Musa ya yi rawan jiki don tsoro, bai kuwa yi karambanin dubawa
ba.

33 “Sa’an nan Ubangiji ya ce masa, ‘Ka cire takalmanka; wurin da kake tsayen nan
mai tsarki ne. 34 Tabbatacce na ga wulaƙancin da ake yi wa mutanena a Masar. Na
ji nishinsu na kuma sauka domin in ’yantar da su. Yanzu ka zo, zan aike ka ka koma
Masar.’*

35 “Wannan Musa ɗin da suka ƙi suna cewa, ‘Wa ya mai da kai mai mulki da kuma
alƙali?’ Allah da kansa ya aike shi, ta wurin mala’ikan da ya bayyana a gare shi a
ɗan itace, yă zama mai mulkinsu, da kuma mai cetonsu. 36 Ya fitar da su daga Masar
ya kuma yi ayyukan da abubuwan banmamaki a Masar, a Jan Teku, da kuma cikin
hamada har shekara arba’in.

37 “Wannan Musa ne ya ce Isra’ilawa, ‘Allah zai aika muku wani annabi kamar ni
daga cikin mutanenku.’† 38 Ya kasance a cikin taron nan a hamada, tare da mala’ikan
da ya yi magana da shi a Dutsen Sinai, da kuma tare da kakanninmu; ya kuma karɓi
kalmomi masu rai don yă miƙa mana.

39 “Amma kakanninmu suka ƙi yin masa biyayya. A maimakon haka, sai suka ƙi
shi a cikin zuciyarsu kuwa suka koma Masar. 40 Suka ce wa Haruna, ‘Ka yi mana
allolin da za su yi mana jagora. Game da wannan Musa ɗin wanda ya fitar da mu
daga Masar, ba mu san abin da ya faru da shi ba!’‡ 41 A lokacin ne suka ƙera gunki
mai siffar ɗan maraƙi. Suka kawo masa hadayu suka kuma yi bikin girmama abin
da suka ƙera da hannuwansu. 42 Sai Amma Allah ya juya musu baya ya kuma ba
da su ga bautar abubuwan da suke a sararin sama. Wannan ya yi daidai da abin da
yake a rubuce a cikin littafin annabawa cewa,

“ ‘Kun kawo mini hadayu da sadakoki
shekaru arba’in cikin, hamada, ya gidan Isra’ila?
43 Kun ɗaukaka gidan tsafin Molek,
da tauraron allahnku Refan,
gumakan da kuka ƙera don ku yi musu sujada.
Saboda haka zan aike ku zuwa bauta’§ gaba da Babilon.

44 “Kakanni-kakanninmu suna da tabanakul na Shaida tare da su a hamada. An yi
shi bisa ga yadda Allah ya umarci Musa, bisa ga zānen da ya gani. 45 Bayan sun gāji
tabanakul nan, kakanninmu a ƙarƙashin jagorancin Yoshuwa suka kawo shi tare
da su, lokacin da suka ƙwace ƙasar daga al’umman da Allah ya kora a idanunsu.
Tabanakul ɗin ya kasance a ƙasar har zamanin Dawuda, 46 wanda ya sami tagomashi
daga Allah, ya kuma nemi yă yi wa Allah na Yaƙub wurin zama. 47 Amma Solomon
ne ya gina masa gida.

48 “Duk da haka, Mafi Ɗaukaka ba ya zama a gidajen da mutane suka gina. Kamar
yadda annabi ya faɗi cewa,
49 “ ‘Sama ne kursiyina,
duniya kuma wurin ajiye tafin ƙafata.

‡ **7:28** Fit 2.14 § **7:32** Fit 3.6 * **7:34** Fit 3.5,7,8,10 † **7:37** M Sh 18.15 ‡ **7:40** Fit 32.1 § **7:43** Amos 5.25

Wane irin gida za ka gina mini?
Ko kuwa ina wurin hutuna zai kasance?
In ji Ubangiji.
50 Ba hannuna ne ya yi dukan waɗannan abubuwa ba?'*
51 "Ku mutane masu taurinkai, da zukata da kuma kunnuwa marasa kaciya! Kuna
kama da kakanninku. Kullum kuna tsayayya da Ruhu Mai Tsarki! 52 An yi wani
annabin da kakanninku ba su tsananta wa ba? Sun ma kashe waɗanda suka yi
maganar zuwan Mai Adalcin nan. Yanzu kuwa kun bashe shi kuka kuma kashe shi
53 ku da kuka karɓi dokar da aka sa a aiki ta wurin mala'iku amma ba ku yi biyayya
da ita ba."

*Jifan Istifanus*

54 Da membobin Sanhedrin suka ji haka, sai suka yi fushi suka ciji haƙoransu.
55 Amma Istifanus, cike da Ruhu Mai Tsarki, ya dubi sama ya kuma ga ɗaukakar
Allah, da Yesu kuma tsaye a hannun dama na Allah. 56 Ya ce, "Ga shi, na ga sama a
buɗe da kuma Ɗan Mutum tsaye a hannun dama na Allah."
57 Da jin haka sai suka tattoshe kunnuwansu, suka kuma yi ihu da ƙarfi sosai, suka
aukar masa gaba ɗaya. 58 Suka ja shi zuwa bayan birnin suka kuma yi ta jifansa
da duwatsu. Ana cikin haka, shaidun suka ajiye tufafinsu a wurin wani saurayi mai
suna Shawulu.
59 Yayinda suke cikin jifansa, sai Istifanus ya yi addu'a ya ce, "Ubangiji Yesu, ka
karɓi ruhuna." 60 Sa'an nan ya durƙusa ya ɗaga murya ya ce, "Ubangiji, kada ka
riƙe wannan zunubi a kansu." Da ya faɗi haka, sai ya yi barci.

# 8

1 Shawulu kuwa yana can, yana tabbatar da mutuwarsa.

*Tsanantawa da warwatsewar ikkilisiya*

A wannan rana wani babban tsanani ya auka wa ikkilisiyar da take a Urushalima,
sai duka suka warwatsu ko'ina a Yahudiya da Samariya, manzanni kaɗai ne suka
rage. 2 Mutane masu tsoron Allah suka binne Istifanus suka kuma yi makoki ƙwarai
dominsa. 3 Amma Shawulu ya fara hallaka ikkilisiya. Yana shiga gida-gida, yana jan
maza da mata yana jefa su cikin kurkuku.

*Filibus a Samariya*

4 Waɗanda aka wartsar suka yi ta wa'azin maganar a duk inda suka tafi. 5 Filibus
ya gangara zuwa wani birni a Samariya ya kuma yi shelar Kiristi a can. 6 Sa'ad da
taron mutane suka ji Filibus suka kuma ga abubuwan banmamakin da ya yi, sai duk
suka mai da hankali sosai ga abin da ya faɗa. 7 Mugayen ruhohi suka fiffito suna
kururuwa daga cikin mutane da yawa, shanyayyu da guragu masu yawa suka sami
warkarwa. 8 Saboda haka aka yi farin ciki ƙwarai a birnin.

*Siman mai sihiri*

9 To, akwai wani mutum mai suna Siman wanda ya kwana biyu yana yin sihiri a
birnin har ya ba wa duk mutanen Samariya mamaki. Ya kuma yi taƙama cewa shi
wani mai girma ne, 10 dukan mutane kuwa, manyan da ƙanana, suka mai da hankali
gare shi suka kuma ce, "Mutumin nan shi ne ikon Allah da aka sani a matsayin Iko
Mai Girma" 11 Suka bi shi domin ya daɗe yana ba su mamaki da sihirinsa. 12 Amma
da suka gaskata da Filibus sa'ad da yake wa'azin labari mai daɗi na mulkin Allah da
kuma sunan Yesu Kiristi, sai aka yi musu baftisma, maza da mata. 13 Siman kansa
ya gaskata aka kuma yi masa baftisma. Ya kuma bi Filibus ko'ina, yana mamakin
manyan alamu da ayyukan banmamakin da ya gani.

* **7:50** Ish 66. 2

14 Sa’ad da manzannin da suke a Urushalima suka ji cewa Samariya ta karɓi
maganar Allah, sai suka aika musu da Bitrus da Yohanna. 15 Da suka iso, sai suka
yi musu addu’a domin su karɓi Ruhu Mai Tsarki, 16 domin Ruhu Mai Tsarki bai riga
ya sauka wa waninsu ba tukuna, an dai yi musu baftisma ne kawai a cikin sunan
Ubangiji Yesu. 17 Sa’an nan Bitrus da Yohanna suka ɗibiya hannuwansu a kansu,
suka kuwa karɓi Ruhu Mai Tsarki.
18 Sa’ad da Siman ya ga cewa ana ba da Ruhu ta wurin ɗibiya hannuwan
manzannin, sai ya miƙa musu kuɗi, 19 ya ce, “Ni ma ku ba ni wannan iyawa don
kowa na ɗibiya wa hannuwana yǎ karɓi Ruhu Mai Tsarki.”
20 Bitrus ya amsa ya ce, “Bari kuɗinka ya hallaka tare da kai, domin ka yi tsammani
za ka iya saya kyautar Allah da kuɗi! 21 Ba ruwanka da wannan hidimar, domin
zuciyarka ba daidai take a gaban Allah ba. 22 Ka tuba daga wannan mugunta ka
kuma yi addu’a ga Ubangiji. Wataƙila zai gafarta maka don irin tunanin da yake a
zuciyarka. 23 Gama na lura kana cike da ɗacin rai kana kuma daure cikin zunubi.”
24 Sai Siman ya amsa ya ce, “Ku yi addu’a ga Ubangiji saboda ni don kada ko ɗaya
daga cikin abin da ka faɗa ya same ni.”
25 Sa’ad da suka yi shaidar suka kuma yi shelar maganar Ubangiji, sai Bitrus da
Yohanna suka koma Urushalima, suna wa’azin bishara a ƙauyukan Samariya masu
yawa.

### *Filibus da mutumin Itiyofiya*

26 To wani mala’ikan Ubangiji ya ce wa Filibus, “Ka yi kudu zuwa hanyar, hanyar
hamada, da ta gangara daga Urushalima zuwa Gaza.” 27 Saboda haka ya kama hanya,
a kan hanyarsa kuwa sai ya sadu da wani mutumin Itiyofiya, wanda yake bābā,
hafsa mai muhimmanci wanda yake lura da dukan ma’ajin Kandas (wanda yake
nufin “sarauniyar mutanen Itiyofiya”). Mutumin nan ya tafi Urushalima ne domin
yin sujada, 28 a kan hanyarsa ta komawa gida kuwa yana zaune bisan keken yaƙinsa
yana karatun littafin annabin Ishaya. 29 Sai Ruhu ya ce wa Filibus, “Matsa wurin
kekunan yaƙin nan ka yi kusa da ita.”
30 Sai Filibus ya ruga zuwa wajen keken yaƙin ya kuma ji mutumin yana karatun
littafin annabin Ishaya. Filibus ya yi tambaya ya ce, “Ka fahimci abin da kake
karantawa?”
31 Sai ya ce, “Ina fa zan iya, in ba dai wani ya fassara mini ba?” Saboda haka sai
ya gayyaci Filibus yǎ hau yǎ zauna tare da shi.
32 Bābān yana karanta wannan Nassin,
“An ja shi kamar tunkiya zuwa mayanka,
kuma kamar ɗan rago a hannun mai askin gashinsa yake shiru,
haka kuwa bai buɗe bakinsa ba.
33 A cikin wulaƙacinsa aka hana masa gaskiya.
Wa zai iya yin zancen zuriyarsa?
Gama an ɗauke ransa daga duniya.”[*]
34 Sai bābān ya tambayi Filibus ya ce, “Ka gaya mini, ina roƙonka, annabin yana
magana a kan wane ne, kansa ne, ko kuwa wani dabam?” 35 Sa’an nan Filibus ya
fara da wannan Nassi ɗin ya kuma faɗa masa labari mai daɗi game da Yesu.
36 Yayinda suke cikin tafiya a kan hanya, sai suka iso wani wurin ruwa bābān nan
ya ce, “Duba, ga ruwa. Me zai hana a yi mini baftisma?”[†] 38 Ya kuwa ba da umarni a
tsai da keken yaƙin. Sa’an nan da Filibus da bābān suka gangara zuwa cikin ruwan
Filibus kuwa ya yi masa baftisma. 39 Sa’ad da suka fita daga cikin ruwan, sai Ruhun

* **8:33** Ish 53.7,8 † **8:36** Waɗansu rubuce-rubucen hannu da da ba su daɗe ba suna da baftisma? 37 Filibus ya ce, “In ka gaskata da dukan zuciyarka, za ka iya.” Bābān ya ce, “Na gaskata cewa Yesu Kiristi shi ne Ɗan Allah.”

Ubangiji ya fyauce Filibus, bābān kuwa bai ƙara ganinsa ba, amma ya ci gaba da
tafiyarsa yana farin ciki. 40 Filibus kuwa ya fito a Azotus, ya yi ta zagawa, yana
wa'azin bishara a dukan garuruwan sai da ya kai Kaisariya.

# 9

### *Tuban Shawulu*
### *(Ayyukan Manzanni 22.6-16; 26.12-18)*

1 Ana cikin haka, Shawulu ya ɗage yana barazana yin kisa da tsananta wa almajiran
Ubangiji. Sai ya je wurin babban firist 2 ya roƙe shi ya ba shi wasiƙu zuwa majami'un
Damaskus, don in ya sami wani a wurin wanda yake bin wannan Hanya, ko maza
ko mata, yǎ kama su a matsayin 'yan kurkuku yǎ kai Urushalima. 3 Da ya yi kusa
da Damaskus a kan hanyarsa, ba zato ba tsammani sai wani haske daga sama ya
haskaka kewaye da shi. 4 Sai ya fāɗi a ƙasa ya kuma ji wata murya ta ce masa,
"Shawulu, Shawulu, don me kake tsananta mini?"
5 Shawulu ya yi tambaya ya ce, "Wane ne kai, ya Ubangiji?"

Ya amsa ya ce, "Ni ne Yesu wanda kake tsananta wa. 6 Yanzu ka tashi ka shiga cikin
birnin, za a kuma gaya maka abin da dole za ka yi."
7 Mutanen da suke tafiya tare da Shawulu suka rasa bakin magana; sun ji muryar
amma ba su ga kowa ba. 8 Shawulu ya tashi daga ƙasa, amma sa'ad da ya buɗe
idanunsa bai iya ganin wani abu ba. Saboda haka aka kama hannunsa aka yi masa
jagora zuwa cikin Damaskus. 9 Kwana uku yana a makance, bai ci ba bai kuma sha
kome ba.
10 A Damaskus kuwa akwai wani almajiri mai suna Ananiyas. Ubangiji ya kira shi
a cikin wahayi ya ce, "Ananiyas!"

Ananiyas ya amsa, "Ga ni, ya Ubangiji."
11 Ubangiji ya ce masa, "Je gidan Yahuda da yake a Miƙaƙƙen Titi ka yi tambaya
ko akwai wani mutum daga Tarshish mai suna Shawulu, gama ga shi yana addu'a.
12 Cikin wahayi ya ga wani mutum mai suna Ananiyas ya zo ya sa hannuwansa a
kansa don yǎ sāke samun ganin gari."
13 Ananiyas ya amsa ya ce, "Ubangiji, na ji labarin mutumin nan sosai da kuma duk
lahanin da ya yi wa tsarkakanka a Urushalima. 14 Ga shi kuma ya zo nan da izinin
manyan firistoci, don yǎ kama duk wanda yake kiran bisa sunanka."
15 Amma Ubangiji ya ce wa Ananiyas, "Je ka! Wannan mutum zaɓaɓɓen kayan
aikina ne don yǎ kai sunana a gaban Al'ummai da sarakunansu da kuma a gaban
mutanen Isra'ila. 16 Zan nuna masa wahalar da dole zai sha saboda sunana."
17 Sa'an nan Ananiyas ya tafi gidan ya kuma shiga ciki. Da ya sa hannuwansa a kan
Shawulu, sai ya ce, "Ɗan'uwana Shawulu, Ubangiji, Yesu, wanda ya bayyana gare ka
a kan hanya yayinda kake zuwa nan, ya aiko ni domin ka sāke gani a kuma cika ka
da Ruhu Mai Tsarki." 18 Nan da nan, sai wani abu kamar ɓawo ya fāɗo daga idanun
Shawulu, ya kuma sāke iya ganin gari. Sai ya tashi aka kuma yi masa baftisma,
19 bayan ya ci abinci, sai sāke samun ƙarfi.

### *Shawulu a Damaskus da Urushalima*

Shawulu ya yi kwanaki masu yawa tare da almajiran da suke a Damaskus. 20 Nan
take ya fara wa'azi cikin majami'u cewa Yesu Ɗan Allah ne. 21 Dukan waɗanda suka
ji shi suka yi mamaki suka ce, "Ba shi ne mutumin da ya tā-da-na-zaune-tsaye a
kan masu kira bisa ga wannan sunan a Urushalima ba? Ba ya zo nan ne don yǎ kai
su a matsayin 'yan kurkuku ga manyan firistoci ba?" 22 Duk da haka Shawulu ya yi
ta ƙara ƙarfi, ya kuma rikitar da Yahudawan da suke zaune a Damaskus, ta wurin
tabbatar musu cewa, Yesu shi ne Kiristi.

23 Bayan kwanaki masu yawa, sai Yahudawa suka haɗa baki su kashe shi, 24 amma
Shawulu ya sami labarin shirinsu. Dare da rana suka yi fakonsa a ƙofofin birnin don
su kashe shi. 25 Amma almajiransa suka ɗauke shi da dare suka saukar da shi a cikin
kwando ta taga a katanga.
26 Da ya zo Urushalima, ya yi ƙoƙarin shiga cikin almajiran amma dukansu suka
ji tsoronsa, ba su gaskata cewa tabbatacce shi almajiri ba ne. 27 Amma Barnabas ya
ɗauke shi ya kawo shi wurin manzanni. Ya gaya musu yadda Shawulu a kan hanyarsa
ya ga Ubangiji kuma cewa Ubangiji ya yi magana da shi, da yadda a Damaskus ya
yi wa'azi ba tsoro a cikin sunan Yesu. 28 Saboda haka Shawulu ya zauna tare da su
yana kai da kawowa a sake a cikin Urushalima, yana magana gabagadi a cikin sunan
Ubangiji. 29 Ya yi magana ya kuma yi muhawwara da Yahudawa masu jin Hellenanci,*
amma suka yi ƙoƙarin kashe shi. 30 Sa'ad da 'yan'uwa suka sami labarin wannan,
sai suka ɗauke shi zuwa Kaisariya suka aika da shi Tarshish.
31 Sa'an nan ikkilisiya ko'ina a Yahudiya, Galili da kuma Samariya ta sami salama.
Ta yi ƙarfi; ta kuma ƙarfafa ta wurin Ruhu Mai Tsarki, ta ƙaru sosai tana rayuwa
cikin tsoron Ubangiji.

### *Eniyas da Dokas*

32 Da Bitrus yake zazzaga ƙasar, sai ya je ya ziyarci tsarkakan da suke a Lidda. 33 A
can ya tarar da wani mutum mai suna Eniyas, shanyayye wanda yake kwance kan
gado shekara takwas. 34 Sai Bitrus ya ce masa, "Eniyas, Yesu Kiristi ya warkar da kai.
Tashi ka naɗe tabarmarka." Nan da nan Eniyas ya tashi. 35 Duk waɗanda suke zama
a Lidda da Sharon suka gan shi suka kuma juyo ga Ubangiji.
36 A Yoffa akwai wata almajira mai suna Tabita (a harshen Girik sunanta shi ne
Dokas†); ita mai aikin alheri ce kullum, tana kuma taimakon matalauta. 37 A lokacin
nan ta yi rashin lafiya ta mutu, aka kuma yi wa gawarta wanka aka ajiye a wani ɗaki
a gidan sama. 38 Lidda yana kusa da Yoffa; saboda haka sa'ad da almajirai suka ji
cewa Bitrus yana a Lidda, sai suka aiki mutum biyu wurinsa su roƙe shi cewa, "In
ka yarda ka zo nan da nan!"
39 Sai Bitrus ya tafi tare da su, sa'ad da ya iso sai aka kai shi ɗakin saman. Duka
gwauraye suka tsaya kewaye da shi, suna kuka suna nunnuna masa riguna da kuma
waɗansu tufafin da Dokas ta yi yayinda take tare da su.
40 Bitrus ya fitar da su duka daga ɗakin; sa'an nan ya durƙusa ya yi addu'a. Da ya
juya wajen matacciyar, sai ya ce, "Tabita, tashi." Ta buɗe idanunta, ta ga Bitrus sai
ta tashi zaune. 41 Ya kama ta a hannu ya taimake ta ta tsaya a ƙafafunta. Sa'an nan
ya kira masu bi da kuma gwaurayen ya miƙa musu ita da rai. 42 Wannan ya zama
sananne ko'ina a Yoffa, mutane da yawa kuma suka gaskata da Ubangiji. 43 Bitrus ya
zauna a Yoffa na ɗan lokaci tare da wani mai aikin fatu mai suna Siman.

# 10

### *Korneliyus ya aika a kira Bitrus*

1 A Kaisariya akwai wani mutum mai suna Korneliyus, wani jarumin Roma ne, a
ƙungiyar soja da ake kira Bataliyar Italiya. 2 Shi da dukan iyalinsa masu ibada ne
masu tsoron Allah kuma; yakan ba da kyauta hannu sake ga masu bukata yana kuma
addu'a ga Allah ba fasawa. 3 Wata rana wajen ƙarfe uku na yamma ya ga wahayi. A
sarari ya ga wani mala'ikan Allah, wanda ya zo wajensa ya ce, "Korneliyus!"
4 Korneliyus kuwa ya zura masa ido a tsorace ya ce, "Mene ne, ya Ubangiji?"

* **9:29** Wato, Yahudawan da suke bin al'adu da yaren Girik. † **9:36** Da Tabita (da Arameyik) da kuma Dokas (da Girik). Suna yana nufin barewa.

Mala'ikan ya ce, "Addu'o'inka da kyautanka ga matalauta sun kai har sama,
hadayar tunawa ce a gaban Allah. 5 Yanzu sai ka aiki mutane zuwa Yoffa su dawo
da wani mutum mai suna Siman wanda ake kira Bitrus. 6 Yana zama tare da Siman,
mai aikin fatu, wanda gidansa ke bakin teku."
7 Sa'ad da mala'ikan da ya yi masa magana ya tafi, sai Korneliyus ya kira biyu daga
cikin bayinsa da kuma wani soja mai ibada wanda yake ɗaya a cikin masu yin masa
hidima. 8 Ya fada musu duk abin da ya faru sa'an nan ya aike su Yoffa.

### *Wahayin Bitrus*

9 Wajen tsakar rana kashegari yayinda suke cikin tafiyarsu suna kuma dab da
birnin, sai Bitrus ya hau bisan rufin gida yǎ yi addu'a. 10 Yunwa ta kama shi ya
kuwa so yǎ ci wani abu, yayinda ake shirya abinci, sai wahayi ya zo masa. 11 Ya ga
sama ya buɗe ana kuwa saukowa wani abu ƙasa kamar babban mayafi zuwa duniya
ta kusurwansa huɗu. 12 Cikinsa kuwa akwai kowace irin dabba mai ƙafa huɗu da
masu ja da ciki na duniya da kuma tsuntsayen sararin sama. 13 Sa'an nan wata murya
ta ce masa, "Bitrus, ka tashi. Ka yanka ka ci."
14 Bitrus ya ce, "Sam, Ubangiji! Ban taɓa cin wani abu marar tsarki ko marar tsabta
ba."
15 Muryar ta yi magana da shi sau na biyu ta ce, "Kada ka ce da abin da Allah ya
tsarkake marar tsarki."
16 Wannan ya faru har sau uku, sai nan da nan aka ɗauke mayafin zuwa sama.
17 Tun Bitrus yana cikin tunani game da ma'anar wahayin nan, sai ga mutanen da
Korneliyus ya aika sun sami gidan Siman suna kuma tsaye a ƙofar. 18 Suka yi sallama,
suna tambaya ko Siman wanda aka sani da suna Bitrus yana zama a can.
19 Yayinda Bitrus yana cikin tunani game da wahayin, sai Ruhu ya ce masa, "Siman,
ga mutum uku* suna nemanka. 20 Saboda haka ka tashi ka sauka. Kada ka yi wata-
wata, gama ni ne na aiko su."
21 Sai Bitrus ya sauka ya ce wa mutanen, "Ni ne kuke nema. Me ya kawo ku?"
22 Mutanen suka amsa, "Mun zo ne daga wurin Korneliyus wani jarumin.
Shi mutum ne mai adalci mai tsoron Allah kuma, wanda dukan Yahudawa ke
girmamawa. Wani mala'ika mai tsarki ya faɗa masa, yǎ sa ka zo gidansa don yǎ
ji abin da za ka faɗa." 23 Sai Bitrus ya gayyaci mutanen cikin gida su zama baƙinsa.

### *Bitrus a gidan Korneliyus*

Kashegari Bitrus ya tafi tare da su, waɗansu 'yan'uwa daga Yoffa kuwa suka tafi
tare da shi. 24 Kashegari sai ya iso Kaisariya. Korneliyus kuwa yana nan yana jiransu,
ya kuma gayyaci 'yan'uwansa da abokansa na kusa. 25 Da Bitrus ya shiga gidan,
Korneliyus ya sadu da shi ya kuma fāɗi a gabansa cikin bangirma. 26 Amma Bitrus
ya sa shi ya tashi. Ya ce, "Tashi, ni mutum ne kawai."
27 Yana magana da shi, sai Bitrus ya shiga ciki ya kuma tarar da taron mutane da
yawa. 28 Sai ya ce musu, "Ku da kanku kun san cewa dokarmu ta hana mutumin
Yahuda yin cuɗanya, ko ya ziyarci Ba'al'umme. Amma Allah ya nuna mini cewa
kada in kira wani mutum marar tsarki ko marar tsabta. 29 Don haka sa'ad da aka
aika in zo, na zo ba wata faɗa. To, ko zan san abin da ya sa ka aika in zo?"
30 Korneliyus ya amsa ya ce, "Kwana huɗu da suka wuce ina a gidana ina addu'a
a wannan lokaci, wajen ƙarfe uku na yamma. Ba zato ba tsammani sai ga wani
mutum cikin tufafi masu walƙiya ya tsaya a gabana 31 ya ce, 'Korneliyus, Allah ya ji
addu'arka, ya kuma tuna da kyautanka ga matalauta. 32 Ka aika zuwa Yoffa don a
kira Siman wanda ake ce da shi Bitrus. Shi baƙo ne a gidan Siman mai aikin fatu,
wanda yake zama a bakin teku.' 33 Saboda haka na aika a zo da kai nan da nan, ya

* **10:19** Wani rubutun hannu na dā biyu; waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā ba su da yawan mutane a nan.

kuma yi kyau da ka zo. To ga mu duka a nan a gaban Allah don mu saurari dukan
abin da Ubangiji ya umarce ka ka faɗa mana."
34 Sa'an nan Bitrus ya fara magana ya ce, "Yanzu na gane yadda gaskiya ne cewa
Allah ba ya sonkai 35 amma yana karɓan mutane daga kowace al'ummar da take
tsoronsa suke kuma aikata abin da yake daidai. 36 Kun san saƙon da Allah ya aika
wa mutanen Isra'ila, yana shelar labari mai daɗi na salama ta wurin Yesu Kiristi,
shi ne kuwa Ubangijin kowa. 37 Kun san abin da ya faru a dukan Yahudiya, farawa
daga Galili bayan baftismar da Yohanna ya yi wa'azi, 38 yadda Allah ya shafe Yesu
Banazare da Ruhu Mai Tsarki da kuma iko, da kuma yadda ya zaga ko'ina yana aikata
alheri yana kuma warkar da dukan waɗanda suke ƙarƙashin ikon Iblis, domin Allah
yana tare da shi.
39 "Mu kuwa shaidu ne na dukan abin da ya yi a ƙasar Yahudawa da kuma a
Urushalima. Suka kashe shi ta wurin rataye shi a kan itace, 40 amma Allah ya tashe
shi daga matattu a rana ta uku, ya sa kuma aka gan shi. 41 Ba dukan mutane ne suka
gan shi ba, amma ta wurin shaidun da Allah ya riga ya zaɓa, ta wurinmu da muka
ci muka kuma sha tare da shi bayan tashinsa daga matattu. 42 Ya umarce mu mu yi
wa'azi ga mutane mu kuma shaida cewa shi ne wanda Allah ya naɗa yă zama mai
shari'a na masu rai da na matattu. 43 Duk annabawa sun yi shaida game da shi cewa
duk wanda ya ba da gaskiya gare shi zai sami gafarar zunubai ta wurin sunansa."
44 Tun Bitrus yana cikin faɗin waɗannan kalmomi, sai Ruhu Mai Tsarki ya sauka
wa duk waɗanda suka ji saƙon. 45 Masu bin da suke da kaciya waɗanda suka zo
tare da Bitrus suka yi mamaki cewa an ba da kyautar Ruhu Mai Tsarki har ma a kan
Al'ummai. 46 Gama sun ji su suna magana da waɗansu harsuna† suna kuma yabon
Allah.
Sai Bitrus ya ce, 47 "Wani zai iya hana a yi wa waɗannan mutane baftisma da
ruwa? Sun karɓi Ruhu Mai Tsarki kamar yadda muka karɓa." 48 Saboda haka ya ba
da umarni a yi musu baftisma cikin sunan Yesu Kiristi. Sa'an nan suka roƙi Bitrus
yă zauna da su na 'yan kwanaki.

# 11

*Bitrus ya bayyana abubuwan da ya yi*

1 Manzanni da 'yan'uwa ko'ina a Yahudiya suka ji cewa Al'ummai ma sun karɓi
maganar Allah. 2 Saboda haka sa'ad da Bitrus ya haura zuwa Urushalima, masu bin
da suke da kaciya suka zarge shi 3 suka ce, "Ka je gidan mutanen da suke marasa
kaciya ka kuwa ci tare da su."
4 Bitrus ya fara yin musu bayani dalla-dalla yadda ya faru cewa, 5 "Ina a birnin
Yoffa ina addu'a, sai ga wahayi ya zo mini. Na ga ana sauko da wani abu kamar
babban mayafi daga sama ta kusurwansa huɗu, ya kuma sauko inda nake. 6 Na duba
cikinsa na ga dabbobi masu ƙafa huɗu na duniya, da namun jeji, da masu ja da ciki,
da kuma tsuntsayen sararin sama. 7 Sa'an nan na ji wata murya tana ce mini, 'Bitrus,
ka tashi. Ka yanka ka ci.'
8 "Na amsa na ce, 'Sam, Ubangiji! Ban taɓa cin wani abu marar tsarki ko marar
tsabta ba.'
9 "Sai muryar daga sama ta yi magana sau na biyu, ta ce, 'Kada ka ce da abin da
Allah ya tsarkake marar tsarki.' 10 Wannan ya faru har sau uku, sa'an nan duk aka
sāke ɗauke shi zuwa sama.
11 "Nan take sai ga mutum uku da aka aika wurina daga Kaisariya a tsaye a ƙofar
gidan da nake. 12 Ruhu ya ce mini kada in yi wata-wata game da tafiya tare da
su. Waɗannan 'yan'uwa guda shida su ma suka rako ni, muka kuwa shiga gidan

† 10:46 Ko Kuwa waɗansu yarurruka

mutumin. 13 Ya kuma gaya mana yadda wani mala'ika ya bayyana a gidansa ya ce
masa, 'Ka aika zuwa Yoffa a kira Siman wanda ake ce da shi Bitrus. 14 Zai kawo maka
saƙo wanda ta wurinsa kai da dukan iyalinka za ku sami ceto.'
15 "Na fara magana ke nan, sai Ruhu Mai Tsarki ya sauko musu yadda ya sauko
mana a farko. 16 Sa'an nan na tuna da abin da Ubangiji ya ce, 'Yohanna ya yi baftisma
da ruwa, amma za a yi muku baftisma da*Ruhu Mai Tsarki.' 17 To, in Allah ya ba su
kyauta yadda ya ba mu, mu da muka gaskata da Ubangiji Yesu Kiristi, wane ni da
zan yi hamayya da Allah?"
18 Sa'ad da suka ji haka, ba su ƙara yin faɗa ba, suka kuma ɗaukaka Allah, suna
cewa, "To, fa, har Al'ummai ma Allah ya sa suka tuba zuwa rai."

### *Ikkilisiya a Antiyok*

19 To, waɗanda suka warwatsu saboda tsananin da ya tashi a kan batun Istifanus
suka tafi har Funisiya, Saifurus da kuma Antiyok, suna ba da saƙon ga Yahudawa
kaɗai. 20 Amma waɗansunsu kuwa, mutane daga Saifurus da Sairin, suka je Antiyok
suka fara yi wa Hellenawa magana su ma, suna ba da labari mai daɗi game da
Ubangiji Yesu. 21 Hannun Ubangiji kuwa yana tare da su, mutane da yawan gaske
kuwa suka gaskata suka juya ga Ubangiji.
22 Labari wannan abu ya kai kunnuwan ikkilisiya a Urushalima, sai suka aiki
Barnabas zuwa Antiyok. 23 Da ya iso ya kuma ga tabbacin alherin Allah, sai ya yi farin
ciki ya kuma ƙarfafa su duka su tsaya da gaskiya cikin Ubangiji da dukan zukatansu.
24 Mutum ne nagari, cike da Ruhu Mai Tsarki da bangaskiya, mutane masu yawan
gaske kuwa suka juya ga Ubangiji.
25 Sa'an nan Barnabas ya tafi Tarshish don yǎ nemi Shawulu, 26 sa'ad da ya same
shi kuwa, sai ya kawo shi Antiyok. Ta haka shekara guda cur Barnabas da Shawulu
suka yi suna taruwa da ikkilisiya, suka kuma koya wa mutane masu yawan gaske. A
Antiyok ne aka fara kiran almajirai da suna Kirista.
27 A wannan lokaci waɗansu annabawa sun zo Antiyok daga Urushalima. 28 Ɗaya
daga cikinsu mai suna Agabus, ya miƙe tsaye ya yi annabci ta wurin Ruhu cewa
za a yi yunwa mai tsanani wadda za tǎ bazu a dukan duniyar Romawa (Wannan
ya faru a zamanin mulkin Kalaudiyus.) 29 Kowanne a cikin almajiran, gwargwadon
azancinsa, ya yanke shawara ya ba da gudummawa ga 'yan'uwan da suke zama a
Yahudiya. 30 Haka kuwa suka yi, suka aika da kyautarsa wa dattawan ikkilisiyar ta
hannu Barnabas da Shawulu.

## 12

### *Kuɓuta mai banmamakin da Bitrus ya yi daga kurkuku*

1 Kusan a wannan lokaci ne Sarki Hiridus ya kama waɗansu da suke na ikkilisiya,
da niyya ya tsananta musu. 2 Ya sa aka kashe Yaƙub, ɗan'uwan Yohanna, da takobi.
3 Sa'ad da ya ga wannan ya faranta wa Yahudawa rai, sai ya kama Bitrus shi ma.
Wannan ya faru kwanakin Bikin Burodi Marar Yisti. 4 Bayan ya kama shi, sai ya sa
shi a kurkuku, ya danƙa shi a hannun soja hurhuɗu kashi huɗu, don su yi gadinsa.
Hiridus ya yi niyyar ya yi masa shari'a a gaban mutane bayan Bikin Ketarewa.
5 Saboda haka aka tsare Bitrus a kurkuku, amma ikkilisiya ta nace da addu'a ga
Allah dominsa.
6 A daren da in gari ya waye da Hiridus yake niyyar kawo shi domin a yi masa
shari'a, Bitrus yana barci tsakanin sojoji biyu, daure da sarƙoƙi biyu, masu gadi
kuma suna bakin ƙofa. 7 Ba zato ba tsammani sai mala'ikan Ubangiji ya bayyana

* **11:16** Ko kuwa a in

haske kuma ya haskaka a ɗakin. Ya bugi Bitrus a gefe ya kuma tashe shi ya ce,
"Maza, ka tashi!" Sarƙoƙin kuwa suka zube daga hannuwansa.
8 Sa'an nan mala'ikan ya ce masa, "Ka sa rigunarka da takalmanka." Bitrus kuwa
ya sa. Mala'ikan ya faɗa masa cewa, "Ka yafa mayafinka ka bi ni." 9 Bitrus ya bi shi
suka fita kurkukun, amma bai ma san cewa abin da mala'ikan yake yi tabbatacce ne
ba; yana tsammani wahayi yake gani. 10 Suka wuce masu gadi na fari da na biyu,
suka kuma isa ƙofar ƙarfe ta shiga birni. Kofar kuwa ta buɗe musu da kanta, suka
kuma wuce. Sa'ad da suka yi tafiya tsawon wani titi, nan take mala'ikan ya bar shi.
11 Sai Bitrus ya dawo hankalinsa ya ce, "Yanzu na sani ba shakka Ubangiji ne
ya aiki mala'ikansa yǎ cece ni daga hannun Hiridus da kuma dukan mugun fatan
Yahudawa."
12 Da ya gane haka, sai ya tafi gidan Maryamu uwar Yohanna, wanda ake kuma
kira Markus, inda mutane da yawa suka taru suna addu'a. 13 Bitrus ya ƙwanƙwasa
ƙofar waje, sai wata mai aiki a gidan da ake kira Roda ta zo tǎ ji ko wane ne. 14 Da
ta gane muryar Bitrus, ta cika da murna ta gudu ta koma ba tare da ta buɗe ƙofar
ba, sai ta koma a guje ta ce da ƙarfi, "Ga Bitrus a bakin ƙofa!"
15 Sai suka ce mata, "Kina hauka." Da ta nace cewa shi ne, sai suka ce, "To, lalle,
mala'ikansa ne."
16 Amma Bitrus ya yi ta ƙwanƙwasawa. Da suka buɗe ƙofar suka kuma gan shi, sai
suka yi mamaki. 17 Bitrus ya yi musu alama da hannunsa su yi shiru sai ya bayyana
yadda Ubangiji ya fitar da shi daga kurkuku. Ya ce, "Ku gaya wa Yaƙub da kuma
'yan'uwa game da wannan," sa'an nan ya tashi ya tafi wani wuri.
18 Da safe, hargitsin da ya tashi tsakanin sojojin ba ƙarami ba ne, a kan abin da
ya sami Bitrus. 19 Bayan Hiridus ya neme shi bai same shi ba, sai ya tuhumi masu
gadin, ya kuma ba da umarni a kashe su.

### *Mutuwar Hiridus*

Sa'an nan Hiridus ya tashi daga Yahudiya ya tafi Kaisariya ya kuma yi 'yan kwanaki
a can. 20 Yana da rashin jituwa da mutanen Taya da na Sidon; sai suka haɗa kai suka
nemi ganawa da shi. Bayan suka sami goyon bayan Bilastus, amintaccen bawan sarki,
sai suka nemi salama, domin sun dogara ga ƙasar sarkin don samun abincinsu.
21 A ranar da aka shirya Hiridus, sanye da kayan sarautarsa, ya zauna a gadon
sarautarsa ya kuma ya wa mutanen jawabi. 22 Suka tā da murya suka ce, "Wannan
muryar wani allah ne, ba ta mutum ba." 23 Nan take, domin Hiridus bai yi wa Allah
yabo ba, wani mala'ikan Ubangiji ya buge shi, tsutsotsi kuwa suka cinye shi ya kuma
mutu.
24 Amma maganar Allah ta ci gaba da ƙaruwa ta kuma bazu.

### *An aiki Barnabas da Shawulu*

25 Sa'ad da Barnabas da Shawulu suka kammala aikinsu, sai suka komo daga*
Urushalima, tare da Yohanna, wanda ake kira Markus.

## 13

1 A ikkilisiyar da take a Antiyok akwai waɗansu annabawa da malamai. Barnabas,
Siman wanda ake kira Baƙi, Lusiyus mutumin Sairin, Manayen (wanda aka goya tare
da Hiridus mai mulki), da kuma Shawulu. 2 Yayinda suna cikin sujada da azumi ga
Ubangiji, Ruhu Mai Tsarki ya ce, "Ku keɓe mini Barnabas da Shawulu domin aikin
da na kira su." 3 Saboda haka bayan suka yi azumi da addu'a, sai suka ɗibiya musu
hannuwansu a kansu suka sallame su.

### *A Saifurus*

* **12:25** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā zuwa

[4] Sai su biyu da Ruhu Mai Tsarki ya aika suka gangara zuwa Selusiya suka shiga
jirgin ruwa daga can zuwa Saifurus. [5] Da suka isa Salamis, sai suka yi shelar maganar
Allah a majami'un Yahudawa. Yohanna yana tare da su a matsayin mai taimakonsu.
[6] Suka zaga dukan tsibirin har sai da suka kai Bafos. A can suka sadu da wani
mutumin Yahuda mai sihiri, annabin ƙarya, mai suna Bar-Yesu, [7] wanda yake
ma'aikacin muƙaddas Sergiyus Bulus ne. Muƙaddas ɗin kuwa mai azanci ne ƙwarai,
ya sa aka kira Barnabas da Shawulu don yana so ya ji maganar Allah. [8] Amma Elimas
mai sihirin nan (domin ma'anar sunansa ke nan) ya yi hamayya da maganarsu ya
kuma yi ƙoƙari ya juyar da muƙaddas ɗin daga bangaskiya. [9] Sai Shawulu, wanda
kuma ake kira Bulus, cike da Ruhu Mai Tsarki, ya kafa wa Elimas ido ya ce, [10] "Kai
ɗan Iblis ne abokin gāban dukan abin da yake daidai! Kana cike da kowane irin ruɗi
da munafunci. Ba za ka daina karkata hanyoyin da suke daidai na Ubangiji ba? [11] Ga
shi hannun Ubangiji yana gāba da kai. Za ka makance, kuma ba za ka ga rana ba
har na wani lokaci."
Nan take, hazo da duhu suka sauko a kansa, ya yi ta lallubawa, yana neman wanda
zai yi masa jagora. [12] Sa'ad da muƙaddas ɗin ya ga abin da ya faru, sai ya ba da
gaskiya, gama ya yi mamaki a kan da koyarwa game Ubangiji.

### *A Antiyok na Fisidiya*

[13] Bulus da abokan tafiyarsa suka tashi daga Bafos a jirgin ruwa zuwa Ferga a
Famfiliya inda Yohanna ya bar su ya koma Urushalima. [14] Daga Ferga kuwa suka
ci gaba zuwa Antiyok na Fisidiya. A ranar Asabbaci sai suka shiga majami'a suka
zauna. [15] Bayan an yi karatu daga cikin Doka, da kuma Annabawa, sai shugabannin
majami'ar suka aika musu suka ce, "'Yan'uwa, in kuna da wani saƙon ƙarfafawa
domin jama'a, sai ku yi."
[16] Yana miƙewa tsaye, sai Bulus ya yi musu alama da hannu ya ce, "Mutanen Isra'ila
da kuma ku Al'ummai da kuke wa Allah sujada, ku saurare ni! [17] Allahn mutanen
Isra'ila ya zaɓi kakanninmu; ya kuma sa mutanen suka yi bunkasa yayinda suke
zama a ƙasar Masar, da iko mai girma ya fitar da su daga ƙasar, [18] ya kuma jure
da halinsu har shekara arba'in a cikin hamada, [19] ya tumɓuke ƙasashe bakwai a
Kan'ana ya kuma ba da ƙasarsu gādo ga mutanensa. [20] Dukan wannan ya ɗauki
kusan shekaru 450.
"Bayan wannan, Allah ya ba su alƙalai har zuwa zamanin annabi Sama'ila. [21] Sa'an
nan mutanen suka nemi a ba su sarki, Allah kuwa ya ba su Shawulu ɗan Kish, na
kabilar Benyamin, wanda ya yi mulki shekaru arba'in. [22] Bayan an kau da Shawulu,
sai ya naɗa Dawuda ya zama sarkinsu. Ya kuma yi shaida game da shi cewa, 'Na
sami Dawuda ɗan Yesse, mutum ne da nake so a zuciyata; shi zai aikata dukan abin
da nake so.'
[23] "Daga zuriyar mutumin nan ne Allah ya kawo wa Isra'ila Mai Ceto Yesu, kamar
yadda ya yi alkawari. [24] Kafin zuwan Yesu, Yohanna ya yi wa'azin tuba da baftisma
ga dukan mutanen Isra'ila. [25] Yayinda Yohanna yake kammala aikinsa ya ce, 'Wa
kuke tsammani ni nake? Ba ni ne shi ba. A'a, amma yana zuwa bayana, wanda ko
takalmansa ma ban isa in kunce ba.'
[26] "Ya ku 'yan'uwa, 'ya'yan Ibrahim, da ku kuma Al'ummai masu tsoron Allah,
a gare mu ne fa aka aiko wannan saƙon ceto. [27] Mutanen Urushalima da masu
mulkinsu ba su gane da Yesu ba, duk da haka cikin hukunta shi suka cika kalmomin
annabawan da ake karantawa kowane Asabbaci. [28] Ko da yake ba su same shi da wani
dalilin da ya kai ga hukuncin kisa ba, suka roƙi Bilatus yǎ sa a kashe shi. [29] Sa'ad
da suka aikata duk abin da aka rubuta game da shi, sai suka saukar da shi daga
itacen suka kuma sa shi a kabari. [30] Amma Allah ya tashe shi daga matattu, [31] kuma

kwanaki da yawa waɗanda suka yi tafiya tare da shi daga Galili zuwa Urushalima suka gan shi. Su ne yanzu shaidu ga mutanenmu.

32 "Muna gaya muku labari mai daɗi cewa abin da Allah ya yi wa kakanninmu
alkawari, 33 ya cika mana, mu zuriyarsu, ta wurin tā da Yesu daga matattu. Kamar
yadda yake a rubuce a cikin Zabura ta biyu cewa,

" 'Kai Ɗana ne,
yau na zama Uba a gare ka.'*

34 Gaskiyar cewa Allah ya tā da shi daga matattu, a kan ba zai taɓa ruɓewa ba, an
faɗe shi a cikin waɗannan kalmomi.

" 'Zan ba ku tsarki da kuma tabbatattun albarkun da na yi wa Dawuda alkawari.'†
35 Haka kuma aka faɗa a wani wuri.
" 'Ba za ka yarda Mai Tsarkinka ya ruɓa ba.'‡

36 "Gama sa'ad da Dawuda ya gama hidimar nufin Allah a zamaninsa, sai ya yi
barci; aka binne shi tare da kakanninsa jikinsa kuwa ya ruɓe. 37 Amma wanda Allah
ya tā da daga matattu bai ruɓa ba.

38 "Saboda haka, 'yan'uwana, ina so ku san cewa ta wurin Yesu ana sanar muku
da gafarar zunubi. 39 Ta wurinsa kowa da ya gaskata an kuɓutar da shi daga dukan
abin da Dokar Musa ba tă iya kuɓutar ba. 40 Ku lura kada abubuwan da annabawa
suka faɗa su faru muku.

41 " 'Ku duba, ku masu ba'a,
ku yi mamaki, ku hallaka,
gama zan yi wani abu a zamaninku
da ba za ku taɓa gaskatawa ba
ko da wani ya gaya muku.'§"

42 Bulus da Barnabas suna fita daga majami'ar ke nan, sai mutane suka gayyace
su su ƙara yin maganan nan a kan waɗannan abubuwa a ranar Asabbaci mai zuwa.
43 Da aka sallami jama'a, Yahudawa da yawa da kuma waɗanda suka tuba suka shiga
Yahudanci masu ibada suka bi Bulus da Barnabas, waɗanda suka yi magana musu
suka kuma ƙarfafa su su ci gaba a cikin alherin Allah.

44 A ranar Asabbaci na biye kusan dukan birnin suka taru don su ji maganar
Ubangiji. 45 Sa'ad da Yahudawa suka ga taron mutanen, sai suka cika da kishi suka
yi ta munanan maganganu a kan abin da Bulus yake faɗi.

46 Sai Bulus da Barnabas suka amsa musu gabagadi, suka ce, "Ya zama mana dole
mu yi muku maganar Allah da farko. Da yake kun ƙi ta ba ku kuma ga kun cancanci
rai madawwami ba, to, za mu juya ga Al'ummai. 47 Gama abin da Allah ya umarce
mu ke nan cewa,

" 'Na sa ka zama haske ga Al'ummai,
don ka kawo cetona zuwa iyakokin duniya.'*"

48 Sa'ad da Al'ummai suka ji haka, sai suka yi farin ciki suka ɗaukaka maganar
Ubangiji; kuma duk waɗanda aka zaɓa don samun rai madawwami, suka gaskata.

49 Maganar Ubangiji kuwa ta bazu a dukan yankin. 50 Amma Yahudawa suka zuga
waɗansu mata masu tsoron Allah masu martaba da kuma waɗansu maza masu
matsayi a gari. Suka tā da tsanani ga Bulus da Barnabas, suka kore su daga yankinsu.
51 Saboda haka suka karkaɗe ƙurar ƙafafunsu don shaidar a kansu suka kuwa tafi
Ikoniyum. 52 Masu bi kuwa suka cika da farin ciki da kuma Ruhu Mai Tsarki.

## 14

### *A Ikoniyum*

* **13:33** Zab 2.7 † **13:34** Ish 55.3 ‡ **13:35** Zab 16.10 § **13:41** Hab 1.5 * **13:47** Ish 49.6

[1] A Ikoniyum Bulus da Barnabas suka shiga majami'ar Yahudawa yadda suka saba.
A can suka yi magana gabagadi har Yahudawa da Al'ummai masu yawa suka gaskata.
[2] Amma Yahudawan da suka ƙi ba da gaskata, suka zuga Al'ummai suka sa ɓata
tsakaninsu da 'yan'uwa. [3] Bulus da Barnabas kuwa suka daɗe sosai a can, suna
magana gabagadi saboda Ubangiji, wanda kuwa ya tabbatar da saƙon alherinsa ta
wurinsa su su aikata ayyuka da alamu masu banmamaki. [4] Mutanen birnin suka
rarrabu, waɗansu suka goyi bayan Yahudawa, waɗansu kuma suka goyi bayan
manzannin. [5] Yahudawa da Al'ummai tare da shugabanninsu suka ƙulla shawara
a tsakaninsu, domin su wulaƙanta su su kuma jajjefe su da duwatsu. [6] Amma suka
sami labari suka kuma gudu zuwa biranen Ikoniyum na Listira da Derbe da kuma
ƙauyukan kewaye, [7] inda suka ci gaba da wa'azin labari mai daɗi.

### *A Listira da Derbe*

[8] A Listira kuwa akwai wani gurgu zaune a ƙafafunsa, wanda gurgu ne tun
haihuwa, kuma bai taɓa tafiya ba. [9] Ya kasa kunne yayinda Bulus yake magana.
Bulus kuma ya kafa masa ido, ya lura cewa yana da bangaskiyar da za tă warkar
da shi [10] sai ya ɗaga murya ya ce, "Tashi ka tsaya kan ƙafafunka!" Da jin haka, sai
mutumin ya yi wuf ya kuma fara tafiya.

[11] Sa'ad da taron suka ga abin da Bulus ya yi, sai suka ihu da harshen Likayoniyawa,
suna cewa, "Alloli sun sauka mana da siffar mutane!" [12] Sai suka ba wa Barnabas,
sunan Zeyus, Bulus kuma suka kira Hermes domin shi ne shugaban magana. [13] Firist
na Zeyus, wanda haikalinsa ke bayan birni, ya kawo bijimai da furanni a ƙofofin
birni domin shi da taron mutanen sun so su miƙa musu hadayu.

[14] Amma da manzannin nan Barnabas da Bulus suka ji haka, sai suka yayyage
tufafinsu suka ruga cikin taron, suna ihu suna cewa, [15] "Ya ku mutane, don me kuke
yin haka? Ai, mu ma mutane ne kawai, 'yan adam ne kamar ku. Mun kawo muku
labari mai daɗi ne, muna gaya muku ku juya daga waɗannan abubuwa banza, ku
juyo ga Allah mai rai, wanda ya yi sama da ƙasa da teku da kuma dukan abin da yake
cikinsu. [16] A zamanin dā, ya bar dukan ƙasashe su yi yadda suka ga dama. [17] Duk da
haka bai bar kansa babu shaida ba. Ya nuna alheri ta wurin ba ku ruwan sama da
kuma amfanin gona a lokutansu; ya ba ku abinci mai yawa ya kuma cika zukatanku
da farin ciki." [18] Ko da waɗannan kalmomi ma, da ƙyar suka hana jama'an nan yin
musu hadaya.

[19] Sai waɗansu Yahudawa suka zo daga Antiyok da Ikoniyum suka sha kan taron.
Suka jajjefi Bulus da duwatsu suka kuma ja shi bayan birni, suna tsammani ya mutu.
[20] Amma bayan da almajiran suka taru kewaye da shi, sai ya tashi ya koma cikin
birni. Kashegari shi da Barnabas suka tashi zuwa Derbe.

### *Komawa zuwa Antiyok a Suriya*

[21] Suka yi wa'azin Labari mai daɗi a wannan birni, suka kuma sami almajirai da
yawa. Sai suka koma Listira, Ikoniyum da kuma Antiyok, [22] suna gina almajirai suna
kuma ƙarfafa su su tsaya da gaske cikin bangaskiya. Suka ce, "Sai da shan wahaloli
masu yawa za mu shiga mulkin Allah." [23] Bulus da Barnabas suka naɗa musu
dattawa* a kowace ikkilisiya, tare da addu'a da azumi, suka miƙa su ga Ubangiji,
wanda suka dogara da shi. [24] Bayan sun bi ta Fisidiya, sai suka zo cikin Famfiliya,
[25] kuma sa'ad da suka yi wa'azi a Ferga, sai suka gangara zuwa Attaliya.

[26] Daga Attaliya kuma suka shiga jirgin ruwa suka koma Antiyok, inda dā aka danƙa
su ga alherin Allah saboda aikin da suka kammala yanzu. [27] Da isarsu a can, sai suka
tara ikkilisiya wuri ɗaya suka ba da rahoton duk abin da Allah ya aikata ta wurinsu

* **14:23** Ko kuwa a Barnabas ya naɗa dattawa; ko kuwa Barnabas ya sa aka naɗa dattawa

da kuma yadda ya buɗe ƙofar bangaskiya domin Al'ummai. 28 Suka kuma jima a can
tare da almajirai.

## 15

*Majalisa a Urushalima*

1 Waɗansu mutane suka gangara daga Yahudiya zuwa Antiyok suna kuma koya wa
'yan'uwa cewa, "Sai ko an yi muku kaciya bisa ga al'ada da Musa ya koyar, in ba haka
ba, ba za ku sami ceto ba." 2 Wannan ya kai Bulus da Barnabas suka shiga babban
gardama da muhawwara da su. Saboda haka aka naɗa Bulus da Barnabas tare da
waɗansu masu bi, su haura zuwa Urushalima don su ga manzanni da dattawa a kan
wannan magana. 3 Ikkilisiya ta raka su suka tafi, yayinda suke ratsawa ta Funisiya
da Samariya, suka ba da labari yadda Al'ummai suka tuba. Wannan labarin ya sa
dukan 'yan'uwa suka yi murna ƙwarai. 4 Sa'ad da suka isa Urushalima, sai ikkilisiya
da manzanni da kuma dattawa suka marabce su, sai suka ba su rahoton dukan abin
da Allah ya aikata ta wurinsu.

5 Sai waɗansu daga cikin masu bin da suke na ƙungiyar Farisiyawa suka miƙe
tsaye suka ce, "Dole ne a yi wa Al'ummai kaciya a kuma bukace su su yi biyayya da
dokokin Musa."

6 Sai manzanni da dattawa suka taru don su duba maganar. 7 Bayan aka yi
muhawwara da sosai, sai Bitrus ya miƙe tsaye ya yi musu jawabi ya ce, "'Yan'uwa,
kun san cewa a kwanakin baya Allah ya yi zaɓe a cikinku don Al'ummai su ji daga
leɓunana saƙon bishara su kuma gaskata. 8 Allah, wanda ya san zuciya, ya nuna
cewa ya karɓe su ta wurin ba su Ruhu Mai Tsarki, kamar yadda ya ba mu. 9 Bai nuna
bambanci tsakaninmu da su ba, gama ya tsarkake zukatansu ta wurin bangaskiya.
10 To, fa, don me kuke ƙoƙari ku gwada Allah ta wurin ɗora wa almajiran nan kayan
da mu ko kakanninmu ba mu iya ɗauka ba? 11 A'a! Mun gaskata cewa ta wurin
alherin Ubangiji Yesu ne muka sami ceto, kamar yadda su ma suka samu."

12 Sai duk taron suka yi tsit yayinda suke sauraron Barnabas da Bulus suna ba
da labari game da ayyuka da kuma abubuwan banmamakin da Allah ya yi a cikin
Al'ummai ta wurinsu. 13 Da suka gama, sai Yaƙub ya yi magana ya ce, "'Yan'uwa, ku
saurare ni. 14 Siman ya bayyana mana yadda Allah da farko ya nuna damuwarsa ta
wurin ɗaukan mutane daga cikin Al'ummai su zama nasa. 15 Kalmomin annabawa
sun yi daidai da wannan, kamar yadda yake a rubuce cewa,

16 " 'Bayan wannan zan koma
in kuma sāke gina tentin Dawuda da ya rushe.
Kufansa zan sāke gina,
in kuma mai da shi,
17 don ragowar mutane su nemi Ubangiji,
kuma duk Al'umman da suke kira bisa sunana,
in ji Ubangiji, wanda yake yin waɗannan abubuwa'*
18 da aka sani tun zamanai.

19 "Saboda haka, a ganina, kada mu matsa wa Al'ummai waɗanda suke juyowa
ga Allah. 20 A maimakon haka, ya kamata mu rubuta musu cewa, su guji abincin
da alloli suka ƙazantar, da fasikanci, da naman dabbar da aka murɗe da kuma jini.
21 Gama Musa ya yi wa'azi a kowace birni tun zamanin dā, ana kuma karanta shi a
majami'u kowane Asabbaci."

*Wasiƙar majalisa zuwa ga al'ummai masu bi*

22 Sai manzanni da dattawa, tare da dukan ikkilisiya, suka yanke shawara su zaɓi
waɗansu daga cikin mutanensu su kuma aike su zuwa Antiyok tare da Bulus da

* **15:17** Amos 9.11,12

Barnabas. Sai suka zaɓi Yahuda (wanda ake kira Barsabbas) da kuma Sila, mutum
biyu da suke shugabanni cikin ʼyanʼuwa. 23 Tare da su suka aika da wannan wasiƙa.
Daga manzanni da dattawa, ʼyanʼuwanku.
Zuwa ga Alʼummai masu bi a Antiyok, Suriya da Silisiya.
Gaisuwa.
24 Mun ji cewa, waɗansu da sun fita daga cikinmu ba tare da izininmu ba suka
kuma dame ku, suna tā da hankalinku ta wurin abin da suka ce. 25 Saboda haka
dukanmu mun yarda mu zaɓi waɗansu mutane mu kuma aike su wurinku tare da
ƙaunatattun abokanmu Barnabas da Bulus 26 mutanen da suka sa rayukansu cikin
hatsari saboda sunan Ubangijinmu Yesu Kiristi. 27 Saboda haka muna aika Yahuda
da Sila don su tabbatar muku da baki abin da muka rubuta. 28 Ya gamshe Ruhu Mai
Tsarki da mu ma kada a ɗora muku nauyi fiye da na waɗannan abubuwa. 29 Ku
guji abincin da aka yi wa alloli hadaya, da jini, da naman dabbar da aka murɗe da
kuma fasikanci. Za ku kyauta in kun kiyaye waɗannan abubuwa.
Ku huta lafiya.
30 Aka sallami mutanen sai suka gangara zuwa Antiyok, inda suka tara ikkilisiya
wuri ɗaya suka ba da wasiƙar. 31 Mutanen suka karantata suka kuma yi farin ciki
saboda saƙonta mai ƙarfafawa. 32 Yahuda da Sila, waɗanda su kansu annabawa
ne, suka yi magana sosai don su gina su kuma ƙarfafa ʼyanʼuwa. 33 Bayan suka
yi ʼyan kwanaki a can, sai ʼyanʼuwa suka sallame su da albarkar salama su dawo
wurin waɗanda suka aike su.† 35 Amma Bulus da Barnabas kuwa suka dakata
a Antiyok, inda su da waɗansu da yawa suka yi koyarwa suka kuma yi waʼazin
maganar Ubangiji.

### *Saɓani tsakanin Bulus da Barnabas*

36 Bayan ʼyan kwanaki sai Bulus ya ce wa Barnabas, "Mu koma mu ziyarci
ʼyanʼuwa a duk garuruwan da muka yi waʼazin bisharar Ubangiji mu ga yadda suke."
37 Barnabas ya so Yohanna, wanda ake kira Markus ya tafi tare da su, 38 amma Bulus
bai ga ya kyautu ya tafi da shi ba, domin ya yashe su a Famfiliya bai kuwa ci gaba tare
da su a aikin ba. 39 Suka sami saɓanin raʼayi tsakaninsu har suka rabu. Barnabas ya
ɗauki Markus suka shiga jirgin ruwa zuwa Saifurus, 40 amma Bulus ya zaɓi Sila suka
kuwa tashi, bayan ʼyanʼuwa suka danƙa su ga alherin Ubangiji. 41 Ya ratsa ta Suriya
da Silisiya, yana ƙarfafa ikkilisiyoyi.

## 16

### *Timoti ya bi Bulus da Sila*

1 Bulus ya kai Derbe saʼan nan kuma zuwa Listira, inda wani almajiri mai suna
Timoti yake da zama, wanda mahaifiyarsa mutuniyar Yahuda ce kuma mai bi ce,
amma mahaifinsa mutumin Hellenawa ne. 2 ʼYanʼuwa a Listira da Ikoniyum sun yi
magana mai kyau ƙwarai a kansa. 3 Bulus ya so ya ɗauke shi a tafiyar, saboda haka
ya yi masa kaciya, domin Yahudawan da suke da zama a wurin, don duk sun san
cewa mahaifinsa mutumin Hellenawa ne. 4 Yayinda suke tafiya daga gari zuwa gari,
suka dinga ba da shawarwarin da manzanni da dattawa a Urushalima suka zartar
domin mutane su kiyaye. 5 Saboda haka ikkilisiyoyi suka ginu cikin bangaskiya suka
kuma yi girma suka yi ta ƙaruwa kowace rana.

### *Wahayin Bulus na mutumin Makidoniya*

6 Bulus da abokan tafiyarsa suka zazzaga dukan yankin Firjiya da Galatiya, don
Ruhu Mai Tsarki ya hana su yin waʼazi a lardin Asiya. 7 Da suka isa kan iyakar Misiya,
suka yi ƙoƙari su shiga Bitiniya, amma Ruhun Yesu bai yarda musu ba. 8 Saboda haka

† **15:33** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da su, 34 amma Sila ya yanke shawara ya dakata a can

suka ratsa Misiya suka zo Toruwas.
9 Da dare Bulus ya ga wahayin wani mutumin
Makidoniya yana tsaye yana roƙonsa cewa, “Ka zo Makidoniya ka taimake mu.”
10 Bayan Bulus ya ga wahayin, muka shirya nan take mu tashi zuwa Makidoniya,
mun tabbata cewa, Allah ya kira mu mu yi musu wa'azin bishara.

### *Tuban Lidiya a Filibbi*

11 Daga Toruwas muka tashi zuwa teku muka kuma shiga jirgin ruwa muka miƙe
kai tsaye zuwa Samotiras, kashegari kuma muka nufi Neyafolis.
12 Daga can muka
tafi Filibbi, wata babbar alkaryar Roma wadda kuma take babban birni a gundumar
Makidoniya. Muka zauna a can kwanaki masu yawa.
13 A Asabbaci, muka fita ƙofar birnin zuwa bakin kogi, inda muke tsammani za mu
sami wurin yin addu'a. Muka zauna muka fara yin wa matan da suka taru a can
magana.
14 Ɗaya daga cikin waɗanda suka saurare mu mace ce mai suna Lidiya, mai
sayar da yadunan jan garura masu tsada daga birnin Tiyatira, mai yi wa Allah sujada.
Ubangiji ya buɗe zuciyarta har ta karɓi saƙon Bulus.
15 Da aka yi mata baftisma tare
da iyalin gidanta, sai ta gayyace mu zuwa gidanta. Ta ce, “In kun amince ni mai bi
ce cikin Ubangiji, sai ku zo ku sauka a gidana.” Sai ta kuwa rinjaye mu.

### *Bulus da Sila a kurkuku*

16 Wata rana muna tafiya zuwa wurin yin addu'a, sai muka sadu da wata baranya
mai ruhun aljani mai duba. Takan samo wa mutanenta kuɗi da yawa, duban da take
yi.
17 Wannan yarinya kuwa ta bi Bulus da kuma sauranmu, tana ihu tana cewa,
“Waɗannan mutane bayin Allah Mafi Ɗaukaka ne, suna sanar da ku hanyar ceto.”
18 Ta yi ta faɗin haka har kwanaki masu yawa. A ƙarshe Bulus ya damu ƙwarai sai
ya juya ya ce wa aljanin, “A cikin sunan Yesu Kiristi na umarce ka, ka rabu da ita!”
Nan take aljanin ya rabu da ita.
19 Da iyayengijin baranyar suka ga hanyar samun kuɗinsu ta toshe, sai suka kama
Bulus da Sila suka ja su zuwa cikin kasuwa don su fuskanci hukuma.
20 Sai suka kawo
su a gaban alƙalai suka ce, “Waɗannan Yahudawa ne, suna kuma birkitar mana da
gari,
21 ta wurin koyar da al'adun da ba daidai ba ne mu Romawa mu karɓa ko mu
aikata.”
22 Sai taron suka fāɗa wa Bulus da Sila gaba ɗaya, alƙalan kuwa suka yi umarni
a tuɓe su a kuma yi musu dūka.
23 Bayan an yi musu bulala sosai, sai aka jefa su
cikin kurkuku, aka umarci mai gadin kurkukun yǎ tsare su da kyau.
24 Da karɓan
irin umarnan nan, sai ya sa su can cikin ɗakin kurkuku na ciki-ciki, kuma ya ɗaura
ƙafafunsu a turu.
25 Wajen tsakar dare Bulus da Sila suna addu'a suna rera waƙoƙi ga Allah, sauran
'yan kurkuku kuwa suna sauraronsu.
26 Ba zato ba tsammani sai aka yi wata babbar
girgizar ƙasa har tushen ginin kurkukun ya jijjiga. Nan da nan sai duk ƙofofin
kurkukun suka bubbuɗe, sarƙoƙin kowa kuma suka ɓaɓɓalle.
27 Mai gadin kurkukun
ya farka daga barci, sa'ad da ya ga ƙofofin kurkukun a buɗe, sai ya zāre takobinsa
yana shirin kashe kansa domin ya ɗauka 'yan kurkukun sun gudu.
28 Amma Bulus
ya yi ihu ya ce, “Kada ka yi wa kanka lahani! Dukanmu muna nan!”
29 Mai gadin kurkukun ya kira a kawo fitilu, ya ruga ciki ya fāɗi yana rawan jiki a
gaban Bulus da Sila.
30 Sai ya fito da su waje ya kuma tambaye su ya ce, “Ranku yǎ
daɗe, me zan yi domin in sami ceto?”
31 Suka amsa suka ce, “Ka gaskata da Ubangiji Yesu, za ka sami ceto, kai da iyalinka.”
32 Sa'an nan suka yi masa maganar Ubangiji shi da kuma dukan sauran da suke a
gidansa.
33 A wannan sa'a na daren, mai gadin kurkukun ya ɗauke su ya wanke
musu raunukansu; nan take aka yi masa baftisma da dukan iyalinsa.
34 Sai mai

gadin kurkukun ya kawo su cikin gidansa ya ba su abinci; ya kuwa cika da murna
don yă gaskata da Allah, shi da dukan iyalinsa.
35 Da gari ya waye, sai alƙalan suka aika ma'aikatansu wajen mai gadin kurkukun
da umarni cewa, “Ka saki mutanen nan.” 36 Sai mai gadin kurkukun ya gaya wa
Bulus cewa, “Alƙalai sun ba da umarni a sake ku kai da Sila. Yanzu sai ku tafi. Ku
sauka lafiya.”
37 Amma Bulus ya ce wa ma'aikatan, “Sun yi mana dūka a fili ba tare da shari'a
ba, ko da yake mu 'yan ƙasar Roma ne, suka kuma jefa mu cikin kurkuku. Yanzu
suna so su fitar da mu a ɓoye? A'a! Sai dai su zo da kansu su rako mu waje.”
38 Sai ma'aikatan suka faɗa wa alƙalan wannan, da suka ji cewa Bulus da Sila
Romawa ne, sai suka ji tsoro. 39 Sai suka zo don su roƙe su, suka yi musu rakiya
daga kurkukun, suna roƙonsu su bar birnin. 40 Bayan Bulus da Sila suka fita daga
kurkukun, sai suka tafi gidan Lidiya, inda suka sadu da 'yan'uwa suka kuma ƙarfafa
su. Sa'an nan suka tafi.

# 17

*A Tessalonika*

1 Da suka bi ta Amfifolis da Afolloniya, sai suka isa Tessalonika, inda akwai
majami'ar Yahudawa. 2 Kamar yadda ya saba, Bulus ya shiga majami'ar, ranakun
Asabbaci uku ya yi ta yin muhawwara da su daga cikin Nassosi, 3 yana musu bayani
da tabbatarwa cewa dole Kiristi ya sha wahala ya kuma tashi daga matattu. Ya kuma
ce, “Wannan Yesu da nake sanar muku shi ne Kiristi.” 4 Waɗansu Yahudawa suka
amince suka kuma bi Bulus da Sila, haka ma Hellenawa da yawa masu tsoron Allah
da kuma manyan mata ba kaɗan ba.
5 Amma Yahudawa suka yi kishi; saboda haka suka tattara 'yan iska daga kasuwa,
suka shirya wata ƙungiya, suka tā da tarzoma a birni. Suka ruga zuwa gidan Yason
suna neman Bulus da Sila don su kawo su a gaban taron. 6 Amma da ba su same su
ba, sai suka ja Yason da waɗansu 'yan'uwa zuwa gaban mahukuntan birnin, suna
ihu suna cewa, “Waɗannan mutanen da suke tā da fitina ko'ina a duniya sun iso nan,
7 Yason kuwa ya karɓe su a gidansa. Dukansu suna karya dokokin Kaisar, suna cewa
akwai wani sarki, wanda ake kira Yesu.” 8 Da suka ji haka, sai hankalin taron da na
mahukuntan birnin ya tashi. 9 Sai suka sa Yason da sauran su biya kuɗin saki sa'an
nan suka sallame su.

*A Bereya*

10 Da dare ya yi, sai 'yan'uwa suka sallami Bulus da Sila su tafi Bereya. Da suka
isa can, sai suka shiga majami'ar Yahudawa. 11 Bereyawa kuwa sun fi Tessalonikawa
hankali, gama sun karɓi saƙon da marmari ƙwarai, suka kuma yi ta yin bincike
Nassosi kowace rana su ga ko abin da Bulus ya faɗa gaskiya ne. 12 Yahudawa da
yawa suka gaskata, haka ma waɗansu manyan matan Hellenawa da kuma mazan
Hellenawa da yawa.
13 Da Yahudawan da suke a Tessalonika suka ji cewa Bulus yana wa'azin maganar
Allah a Bereya, sai suka je can ma, suna zuga taro suna kuma tā da hankalinsu. 14 Nan
da nan 'yan'uwa suka sa Bulus yă tafi bakin teku, amma Sila da Timoti suka dakata
a Bereya. 15 Mutanen da suka raka Bulus kuwa suka kawo shi Atens sa'an nan suka
dawo da umarnai wa Sila da Timoti cewa su zo wurinsa da gaggawa.

*A Atens*

16 Yayinda Bulus yake jiransu a Atens, ya damu ƙwarai da ya ga birnin cike da
gumaka. 17 Saboda haka ya yi ta muhawwara a majami'a da Yahudawa da kuma
Hellenawa masu tsoron Allah, haka kuma da waɗanda yake tararwa a bakin kasuwa.

18 Wata ƙungiyar Afikuriya da kuma masu bin ussan ilimin Sitoyik suka fara gardama
da shi. Waɗansunsu suka ce, "Mene ne mai surutun nan yake ƙoƙarin faɗi?"
Waɗansu suka ce, "Kamar yana wa'azin baƙin alloli ne." Sun faɗa haka ne domin
Bulus yana wa'azin labari mai daɗi game da Yesu da kuma tashin matattu. 19 Sai suka
ɗauke shi suka kawo shi wurin taron Areyofagus, inda suka ce masa, "Ko za mu san
mene ne sabon koyarwan nan ya ƙunsa da kake yi? 20 Kana kawo mana ra'ayoyin da
suke baƙo a gare mu, kuma muna so mu san mene ne suke nufi." 21 (Duk Atenawa
da baƙin da suke zama a can suna zaman kashe wando ne kawai kuma ba abin da
suke yi sai dai tafi da kuma jin sababbin ra'ayoyi.)

22 Sai Bulus ya miƙe tsaye a tsakiyar taron Areyofagus ya ce, "Ya ku mutanen Atens!
Na dai lura cewa ta kowace hanya ku masu addini ne ƙwarai. 23 Gama sa'ad da nake
zagawa, na lura da kyau da abubuwan da kuke bauta wa, har ma na tarar da wani
bagade da wannan rubutu,

Ga Allahn da ba a sani ba.

To, abin nan da kuke yi wa sujada a matsayin abin da ba ku sani nan ba shi ne zan
sanar da ku.

24 "Allahn da ya halicci duniya da kome da yake cikinta shi ne Ubangijin sama
da ƙasa, ba ya kuma zama a haikalin da aka gina da hannuwa. 25 Ba a kuma yin
masa hidima da hannun mutum, sai ka ce mai bukatan wani abu, domin shi kansa
ne ke ba wa dukan mutane rai da numfashi da kuma kome. 26 Daga mutum ɗaya,
ya halicci kowace al'ummar mutane, don su zauna a duk duniya; shi ne kuma ya
ƙaddara lokuta bisa ga tsarinsu da kuma inda za su kasance. 27 Allah ya yi wannan
domin mutane su neme shi mai yiwuwa kuma su lalluba su same shi, ko da yake
ba shi da nisa daga kowannenmu. 28 'Gama a cikinsa ne muke rayuwa muke motsi
muka kuma kasance.' Yadda waɗansu mawaƙanku suka ce, 'Mu zuriyarsa ce.'

29 "Saboda haka da yake mu zuriyar Allah ce, kada mu yi tsammani cewa kamannin
Allah yana kama da zinariya ko azurfa ko dutse, siffar da mutum ya ƙago ta wurin
dabarabarsa. 30 A dā Allah ya kawar da Allah ya kawar da kai ga zamanin jahilci, amma
yanzu ya umarci dukan mutane a ko'ina su tuba. 31 Gama ya sa ranar da zai yi wa
duniya shari'a da adalci ta wurin mutumin da ya naɗa. Ya riga ya ba da tabbacin
wannan ga dukan mutane ta wurin tā da shi daga matattu."

32 Sa'ad da suka ji maganar tashin matattu, waɗansunsu suka yi tsaki, amma
waɗansu suka ce, "Muna so mu ƙara jin ka a kan wannan batu." 33 Da wannan,
Bulus ya bar Majalisar. 34 Waɗansu mutane kima suka zama mabiyan Bulus suka
kuwa gaskata. A cikinsu kuwa akwai Diyonasiyus ɗan Majalisar Areyofagus, haka
kuma wata mace mai suna Damaris, da waɗansu dai haka.

# 18

*A Korint*

1 Bayan haka, Bulus ya bar Atens ya tafi Korint. 2 A can ya sadu da wani mutumin
Yahuda mai suna Akwila, ɗan garin Fontus, wanda ya je can ba da daɗewa ba daga
Italiya tare da matarsa Firiskila, gama Kalaudiyus ya umarci dukan Yahudawa su bar
Roma. Sai Bulus ya tafi yă gan su, 3 da yake shi ma mai ɗinkin tenti ne kamar su,
sai ya zauna ya yi aiki tare da su. 4 Kowace Asabbaci kuwa yakan yi muhawwara a
majami'a, yana ƙoƙari yă rinjayi Yahudawa da Hellenawa.

5 Sa'ad da Sila da Timoti suka iso daga Makidoniya, sai Bulus ya ba da kansa ga yin
wa'azi kaɗai, yana tabbatar wa Yahudawa cewa Yesu shi ne Kiristi. 6 Amma sa'ad
da Yahudawa suka yi hamayya da Bulus suka kuma shiga zaginsa, sai ya karkaɗe
tufafinsa a cikin rashin yarda, ya ce musu, "Alhakinku yana a kanku! Ba ni da wani
laifi. Daga yanzu zan tafi wajen Al'ummai."

7 Sai Bulus ya bar majami'ar ya kuma tafi ƙofar da take kusa da gidan Titus Yustus,
mai yi wa Allah sujada. 8 Kirisbus, shugaban majami'a, da dukan iyalinsa suka
gaskata Ubangiji; Korintiyawa masu yawa kuwa da suka ji shi suka gaskata, aka
kuwa yi musu baftisma.
9 Wata rana da dad dare, Ubangiji ya yi magana da Bulus a cikin wahayi ya ce,
"Kada ka ji tsoro; ka ci gaba da yin magana, kada ka yi shiru. 10 Gama ina tare da
kai, ba kuma wanda zai fāɗa maka ya cuce ka, domin ina da mutane da yawa a
wannan birni." 11 Saboda haka Bulus ya zauna a nan har shekara ɗaya da rabi, yana
koya musu maganar Allah.
12 Yayinda Galliyo yake muƙaddas Akayya, Yahudawa suka haɗa kai suka tasar wa
Bulus, suka kuwa kawo shi cikin kotu. 13 Suka yi zarge cewa, "Wannan mutum yana
rarrashin mutane su yi wa Allah sujada a hanyoyin da suka saɓa wa doka."
14 A daidai sa'ad da Bulus yana shirin yin magana, sai Galliyo ya ce wa Yahudawan,
"Da a ce ku Yahudawa kuna gunaguni game da munafunci, ko kuma wani babban
laifi, da sai in iya sauraronku. 15 Amma da yake ya shafi gardama ce game da kalmomi
da sunaye da kuma dokarku, sai ku ji da ita da kanku. Ni ba zan zama mai shari'a
kan irin waɗannan abubuwa ba." 16 Saboda haka ya kore su. 17 Sai duk suka juya
kan Sostenes shugaban majami'a suka yi masa dūka a gaban kotun. Amma Galliyo
ko yă kula.

### *Firiskila, Akwila da Afollos*

18 Bulus kuwa ya ci gaba da zama a Korint na 'yan kwanaki. Sa'an nan ya bar
'yan'uwa ya shiga jirgin ruwa zuwa Suriya tare da Firiskila da Akwila. Kafin ya tashi,
ya aske kansa a Kenkireya saboda alkawarin da ya yi. 19 Suka isa Afisa, inda Bulus
ya bar Firiskila da Akwila. Shi kansa ya shiga majami'a ya kuma yi muhawwara
da Yahudawa. 20 Sa'ad da suka roƙe shi ya ƙara 'yan kwanaki da su, bai yarda ba.
21 Amma da yake barin wurin, ya yi alkawari cewa, "Zan dawo in Allah ya yarda."
Sa'an nan ya tashi daga Afisa a jirgin ruwa. 22 Sa'ad da ya sauka a Kaisariya, sai ya
haura ya gai da ikkilisiya sa'an nan ya gangara zuwa Antiyok.
23 Bayan ya yi 'yan kwanaki a Antiyok, Bulus ya tashi daga can ya zaga ko'ina a
yankin Galatiya da Firjiya, yana ƙarfafa dukan almajirai.
24 Ana cikin haka sai wani mutumin Yahuda mai suna Afollos, ɗan ƙasar
Alekzandariya, ya zo Afisa. Shi masani ne, yana da cikakken sani na Nassosi. 25 An
horar da shi a hanyar Ubangiji, ya kuma himma ƙwarai a magana, ya kuma yi
koyarwa game da Yesu, daidai, ko da yake baftismar Yohanna ce kaɗai ya sani. 26 Sai
ya fara magana gabagadi a majami'a. Sa'ad da Firiskila da Akwila suka ji shi, sai
suka gayyace shi gidansu suka ƙara bayyana masa hanyar Allah sosai.
27 Sa'ad da Afollos ya so ya tafi Akayya, sai 'yan'uwa suka ƙarfafa shi suka kuma
rubuta wa almajiran da suke can da su marabce shi. Da isowarsa, ya zama da taimako
ƙwarai ga waɗanda ta wurin alheri suka gaskata. 28 Gama da ƙwazo ya ƙaryata
Yahudawa a muhawwara a fili, yana tabbatar daga Nassosi cewa Yesu shi ne Kiristi.

## 19

### *Bulus a Afisa*

1 Lokacin da Afollos yake a Korint, Bulus ya bi hanyar da ta ratsa ta Asiya ya zo
Afisa. A can ya sadu da waɗansu almajirai, 2 sai ya tambaye, su ya ce, "Kun karɓi
Ruhu Mai Tsarki sa'ad da kuka gaskata?"
Suka amsa suka ce, "A'a, ba mu ma san akwai Ruhu Mai Tsarki ba."
3 Saboda haka Bulus ya yi tambaya ya ce, "To, wace baftisma aka yi muku?"
Suka ce, "Baftismar Yohanna."

4 Bulus ya ce, "Ai, baftismar Yohanna, baftisma ce ta tuba. Ya ce wa mutane su
gaskata a wani wanda yake zuwa bayansa, wato, Yesu." 5 Da ji wannan, sai aka yi
musu baftisma a cikin sunan Ubangiji Yesu. 6 Da Bulus ya ɗibiya musu hannuwansa,
sai Ruhu Mai Tsarki ya sauka musu, suka kuwa yi magana da harsuna, suka kuma yi
annabci. 7 Mutane kuwa su wajen mutum goma sha biyu ne.

8 Bulus ya shiga majami'a ya yi magana gabagadi a can na watanni uku, yana
muhawwara yana kuma rinjayarsu game da mulkin Allah. 9 Amma waɗansunsu
suka taurara; suka ƙi su gaskata kuma a gaban jama'a suka yi baƙar magana game
da Hanyar. Bulus kuwa ya bar su. Ya tafi tare da almajirai ya dinga tattaunawa da
su kullum a babban ɗakin jawabi na Tirannus. 10 Wannan ya ci gaba har shekara
biyu, sai da ya sa dukan Yahudawa da Hellenawa da suke zaune a lardin Asiya suka
ji maganar Ubangiji.

11 Allah ya yi ayyukan banmamakin da suka wuce misali ta hannu Bulus, 12 har ma
ana kai hankicif da adikan da suka taɓa jikinsa wa marasa lafiya, suka kuwa warke
daga cututtukansu mugayen ruhohi kuma suka rabu da su.

13 Waɗansu Yahudawa masu yawo gari-gari suna fitar da mugayen ruhohi suka yi
ƙoƙari su yi amfani da sunan Ubangiji Yesu a kan waɗanda suke da aljanu. Suna
cewa, "A cikin sunan Yesu wanda Bulus yake wa'azi, na umarce ku, ku fito." 14 'Ya'ya
bakwai maza na Sikeba, wani babban firist na Yahudawa, suna yin haka. 15 Wata rana
mugun ruhu ya amsa musu ya ce, "Yesu kam na sani, Bulus kuma na sani, amma ku
kuma su wane ne?" 16 Sai mutumin da yake da mugun ruhun ya fāɗa musu ya sha
ƙarfinsu duka. Ya yi musu dūkan tsiya har suka fita a guje daga gidan tsirara jini
yana zuba.

17 Da Yahudawa da Hellenawan da suke zama a Afisa suka ji wannan labari sai
duk tsoro ya kama su, aka kuwa darjanta sunan Ubangiji Yesu ƙwarai. 18 Da yawa
cikin waɗanda suka gaskata yanzu suka zo a fili suka furta mugayen ayyukansu.
19 Waɗansu masu yin sihiri suka kawo naɗaɗɗun littattafansu wuri ɗaya suka kuwa
ƙone su a gaban jama'a. Sa'ad da aka lissafta yawan kuɗin naɗaɗɗun littattafan nan,
sai jimillar ta kai darik dubu hamsin. 20 Ta haka maganar Ubangiji ta bazu ko'ina ta
kuma yi ƙarfi.

21 Bayan dukan wannan ya faru, sai Bulus ya yanke shawara ya ratsa Makidoniya
da Akayya in za shi Urushalima. Ya kuma ce, "Bayan na tafi can, dole in ziyarci
Roma ita ma." 22 Sai ya aiki biyu daga cikin masu taimakonsa, Timoti da Erastus,
zuwa Makidoniya, yayinda shi kuwa ya ɗan dakata a lardin Asiya.

### *Hargitsi a Afisa*

23 Kusan wannan lokaci sai aka yi wani babban hargitsi game da wannan Hanyar.
24 Wani maƙerin azurfa, mai suna Demetiriyus wanda yake ƙera siffar ɗakunan tsafin
Artemis da azurfa, ba ƙaramin ciniki yake kawo wa mutane masu sana'an nan ba.
25 Sai ya tara su wuri ɗaya, tare da masu irin wannan sana'ar ya ce, "Ku jama'a, kun
san muna samun kuɗin shiga sosai daga wannan sana'a. 26 Kuma kuna ji kuna gani
yadda Bulus ɗin nan ya shawo kan mutane da yawa ya kuma sa suka bauɗe a nan
a Afisa da dukan lardin Asiya. Yana cewa alloli da mutum ya ƙera ba alloli ba ne
ko kaɗan. 27 Akwai hatsari, ba kawai cewa sana'armu za tă rasa sunanta mai daraja
ba, amma za a yi banza da ɗakin tsafin Artemis alliyarmu mai girma, alliyar kanta
wadda ake bauta a ko'ina a yankin Asiya da kuma duniya, za a raba ta da darajarta."

28 Da suka ji haka, sai suka yi fushi ƙwarai suka fara ihu suna cewa, "Girma ta
tabbata ga Artemis ta Afisawa!" 29 Jim kaɗan sai hayaniya ta tashi a dukan birnin.
Sai mutane suka cafke Gayus da Aristarkus, abokan tafiyar Bulus daga Makidoniya,
suka ruga da zuwa fili da nufi ɗaya. 30 Bulus ya so ya bayyana a gaban taron, amma

almajirai ba su bar shi ba. 31 Har waɗansu shugabannin lardin ma, abokan Bulus,
suka aika masa suna roƙonsa kada yǎ kuskura ya shiga filin nan.
32 Taron kuwa ya ruɗe. Waɗansu suna ihu suna ce abu kaza, waɗansu kuma wani
abu dabam. Yawancin mutane kuma ba su ma san abin da ya sa suke a wurin ba.
33 Yahudawa suka tura Alekzanda gaba, sai waɗansu a taron suka riƙa yin masa ihu.
Sai ya ɗaga hannu don a yi shiru don yǎ kāre kansa a gaban mutane. 34 Amma sa'ad
da suka gane shi mutumin Yahuda ne, sai duk suka yi ihu gaba ɗaya na kusa sa'a
biyu, suna cewa, "Girma ta tabbata ga Artemis ta Afisawa!"
35 Sai magatakardar birnin ya sa taron su yi shiru, sa'an nan ya ce, "Mutanen
Afisa, ashe duk duniya ba tǎ san cewa birnin Afisa ce mai lura da haikalin Artemis
mai girma da kuma siffarta da ya fāɗi daga sama ba? 36 Saboda haka, da yake ba
dama a yi mūsun wannan gaskiya, ya kamata ku natsu kada ku yi kome da garaje.
37 Kun kawo mutanen nan a nan, gashi kuwa ba su yi fashin haikali ba, ba su kuwa
saɓa wa alliyarmu ba. 38 To, in haka ne, in Demetiriyus da abokan sana'arsa suna da
wata magana game da wani ai, kotuna suna nan a buɗe, akwai kuma muƙaddasai.
Suna iya kai ƙara. 39 In kuma akwai wani abu har yanzu da kuke so ku kawo, dole
a daidaita shi a majalisa. 40 Yadda yake a yanzu, muna a hatsarin amsa zargin ta da
hargitsi saboda abin da ya faru yau. Da yake ba za mu iya ba da dalilin da ya sa aka
yi wannan hargitsi ba." 41 Bayan da ya faɗi haka, sai ya sallami taron.

# 20

*Bulus ya ratsa Makidoniya da Giris*

1 Sa'ad da hayaniyar ta kwanta, sai Bulus ya aika a kira almajiran, kuma bayan
ya ƙarfafa su, sai ya yi bankwana ya tafi Makidoniya. 2 Ya ratsa wurin yana ƙarfafa
mutanen da kalmomi masu yawa, a ƙarshe kuma ya kai Giris, 3 inda ya zauna wata
uku. Da yake Yahudawa sun ƙulla masa makirci, a lokacin da yake shirin tashi
cikin jirgin ruwa zuwa Suriya, sai ya yanka shawara yǎ koma ta Makidoniya. 4 Sai
Sofater ɗan Fairrus daga Bereya, Aristarkus da Sekundus daga Tessalonika, Gayus
daga Derbe, Timoti ma, da Tikikus da Turofimus daga lardin Asiya suka tafi tare da
shi. 5 Waɗannan mutane suka sha gaba suka kuma jira mu a Toruwas. 6 Amma muka
tashi daga Filibbi a jirgin ruwa bayan Bikin Burodi Marar Yisti bayan kuma kwana
biyar muka sadu da sauran a Toruwas, inda muka zauna kwana bakwai.

*Ta da Yutikus daga matattu a Toruwas*

7 A ranar farko ta mako muka taru wuri ɗaya don gutsuttsura burodi. Bulus ya
yi wa mutane magana, don yana niyyar tashi kashegari, sai ya yi ta yin magana har
tsakar dare. 8 Akwai fitilu da yawa a ɗakin gidan saman da muka taru. 9 Akwai wani
saurayi zaune a taga mai suna Yitikus, wanda barci mai nauyi ya ɗauke shi yayinda
Bulus yake ta tsawaita magana. Sa'ad da yake barci, sai ya fāɗi daga gidan sama
a hawa ta uku aka kuma ɗauke shi matacce. 10 Sai Bulus ya sauka, ya miƙe a kan
saurayin ya rungume shi ya ce, "Kada ku damu, yana da rai!" 11 Sai ya koma ɗakin
da yake a gidan sama, ya gutsuttsura burodi ya kuma ci. Bayan ya yi magana har
gari ya waye, sai ya tafi. 12 Mutanen suka ɗauki saurayin da rai zuwa gida suka kuma
ta'azantu ƙwarai da gaske.

*Bankwanan Bulus ga dattawan Afisa*

13 Mu kuwa muka ci gaba zuwa jirgin ruwan muka tashi muka nufi Assos inda
za mu ɗauki Bulus. Ya yi wannan shirin don zai tafi can da ƙafa. 14 Da ya same
mu a Assos, sai muka ɗauke shi a jirgin ruwan muka zo Mitilen. 15 Kashegari muka
tashi cikin jirgin ruwa daga can muka zo gefen Kiyos. Kwana ɗaya bayan wannan,

sai muka ƙetare zuwa Samos, kashegari kuma muka iso Miletus. 16 Bulus ya yanke
shawara yă wuce Afisa a jirgin ruwa don kada yă ɓata lokaci a lardin Asiya, gama
yana sauri yă kai Urushalima, in ya yiwu ma, a ranar Fentekos.

17 Daga Miletus, Bulus ya aika zuwa Afisa a kira dattawan ikkilisiya. 18 Da suka iso,
sai ya ce musu, “Kun san irin zaman da na yi tun lokacin da na zauna da ku, daga
ranar farkon da na zo cikin lardin Asiya. 19 Na bauta wa Ubangiji da matuƙar tawali’u
har da hawaye, da gwagwarmaya iri-irin da na sha game da makircin Yahudawa.
20 Kun san cewa ban yi wata-wata yin muku wa’azi game da duk abin da zai amfane
ku ba amma na koyar da ku a fili da kuma gida-gida. 21 Na yi shela ga Yahudawa da
Hellenawa cewa dole su juye ga Allah cikin tuba su kuma amince da Ubangijinmu
Yesu.

22 “Yanzu kuma Ruhu ya tilasta ni, za ni Urushalima, ba tare da sanin abin da
zai faru da ni a can ba. 23 Na dai san cewa a kowace birni Ruhu Mai Tsarki yakan
gargaɗe ni cewa kurkuku da shan wuya suna jirana. 24 Amma ni ban ɗauki raina a
bakin kome ba, in dai zan iya gama tserena in kuma kammala aikin da Ubangiji Yesu
ya ba ni aikin shaida bisharar alherin Allah.

25 “Yanzu na san cewa ba ko ɗaya daga cikinku wanda na zazzaga ina muku wa’azin
mulkin Allah da zai sāke ganina. 26 Saboda haka, ina muku shela a yau cewa ba ni
da alhakin kowa a kaina. 27 Gama ban yi wata-wata a sanar muku dukan nufin Allah
ba. 28 Ku lura da kanku da dukan garken da Ruhu Mai Tsarki ya sa ku ku zama masu
kula da shi. Ku zama masu kiwon ikkilisiyar Allah, wadda ya saya da jininsa. 29 Na
san cewa bayan na tafi, mugayen kyarketai za su shigo cikinku ba za su kuwa ƙyale
garken ba. 30 Ko cikinku ma mutane za su taso su karkatar da gaskiya don su jawo
wa kansu almajirai. 31 Saboda haka ku zauna a faɗake! Ku tuna cewa shekara uku,
dare da rana ban taɓa fasa yin wa kowannenku gargaɗi ba, har da hawaye.

32 “To, yanzu na danƙa ku ga Allah da kuma ga maganar alherinsa, wadda za tă
iya gina ku ta kuma ba ku gādo a cikin dukan waɗanda aka tsarkake. 33 Ban yi
ƙyashin azurfa ko zinariya ko tufafin kowa ba. 34 Ku kanku kun san cewa hannuwan
nan nawa sun biya mini bukatuna da kuma na abokan aikina. 35 Cikin kowane abin
da na yi, na nuna muku cewa da irin wannan aiki tuƙuru don mu taimaki marasa
ƙarfi, muna tunawa da kalmomin da Ubangiji Yesu kansa ya ce, ‘Bayarwa ta fi karɓa
albarka.’ ”

36 Da ya faɗi haka, ya durƙusa tare da dukansu ya yi addu’a. 37 Sai dukansu suka
yi kuka suka rungume shi, suka kuma yi masa sumba. 38 Abin da ya fi sa su baƙin
ciki shi ne maganarsa da ya ce, ba za su ƙara ganin fuskarsa ba. Sai suka raka shi
zuwa wajen jirgin ruwa.

# 21

*Zuwa Urushalima*

1 Bayan muka rabu da su da ƙyar, sai muka shiga jirgin ruwa, muka miƙe zuwa
Kos. Kashegari muka tafi Rods daga can kuma muka je Fatara. 2 Sai muka sami wani
jirgin ruwa da zai ƙetare zuwa Funisiya, sai muka shiga muka kama tafiya. 3 Bayan
muka hangi Saifurus muka wuce shi ta kudu, sai muka ci gaba zuwa Suriya. Muka
sauka a Taya, inda jirgin ruwanmu zai sauke kayansa. 4 Da muka sami almajirai a
can, sai muka zauna da su kwana bakwai. Ta wurin Ruhu, suka yi ƙoƙari su hana
Bulus wucewa zuwa Urushalima. 5 Amma da lokacin tashinmu ya yi, sai muka tashi
muka ci gaba da tafiyarmu. Dukan almajirai da matansu da ’ya’yansu suka raka mu
har bayan birni, a can kuwa a bakin teku muka durƙusa muka yi addu’a. 6 Bayan
mun yi bankwana da juna, sai muka shiga jirgin ruwa, su kuwa suka koma gida.

7 Muka ci gaba da tafiyarmu daga Taya muka sauka a Tolemayis, inda muka gai da
ʼyanʼuwa muka yi kwana ɗaya tare da su. 8 Da muka tashi kashegari, sai muka isa
Kaisariya muka kuma sauka a gidan Filibus mai bishara, ɗaya daga cikin Bakwai ɗin
nan. 9 Yana da ʼyaʼya huɗu ʼyan mata da ba su yi aure ba, waɗanda suka yi annabci.
10 Bayan muka yi ʼyan kwanaki da dama a can, sai wani annabin da ake kira Agabus
ya gangaro daga Yahudiya. 11 Da ya zo wurinmu, sai ya ɗauki ɗamarar Bulus, ya
ɗaura hannuwansa da ƙafafunsa da ita saʼan nan ya ce, "Ruhu Mai Tsarki ya ce,
'Haka Yahudawan Urushalima za su daure mai wannan ɗamara su kuma ba da shi
ga Alʼummai.' "
12 Saʼad da muka ji haka, sai mu da mutanen da suke can muka roƙi Bulus kada
yă je Urushalima. 13 Sai Bulus ya amsa ya ce, "Don me kuke kuka kuna kuma ɓata
mini zuciya? A shirye nake ba ma a daure ni kawai ba, amma har ma in mutu a
Urushalima saboda sunan Ubangiji Yesu." 14 Da dai ya ƙi rarrasuwa, muka yi shiru,
muka ce, "Bari Ubangiji yă yi nufinsa."
15 Bayan haka, sai muka shirya muka kuma haura zuwa Urushalima. 16 Waɗansu
almajirai daga Kaisariya suka raka mu suka kawo mu gidan Minason, inda za mu
sauka. Shi mutumin Saifurus ne kuma ɗaya daga cikin almajirai na farko.

### *Isowar Bulus a Urushalima*

17 Saʼad da muka zo Urushalima, ʼyanʼuwa suka karɓe mu da murna. 18 Kashegari
Bulus da sauranmu muka tafi domin mu ga Yaƙub, dukan dattawan kuwa suna nan.
19 Bulus ya gaishe su ya kuma ba su rahoto dalla-dalla a kan abin da Allah ya yi a
cikin Alʼummai ta wurin aikinsa.
20 Da suka ji haka, sai suka yabi Allah. Saʼan nan suka ce wa Bulus, "Ka gani
ɗanʼuwa, yawan dubban Yahudawan da suka gaskata, kuma dukansu masu himma
ne a wajen bin doka. 21 An sanar da su cewa kana koya wa dukan Yahudawan da
suke zama a cikin Alʼummai cewa su juye daga Musa, kana kuma faɗa musu kada
su yi wa ʼyaʼyansu kaciya ko su yi rayuwa bisa ga alʼadunmu. 22 To, me za mu yi
ke nan? Lalle za su ji cewa ka iso, 23 saboda haka, ka yi abin da muka faɗa maka.
Akwai mutum huɗu tare da mu da suka yi alkawari. 24 Ka ɗauki waɗannan mutane,
ka tafi da su ku tsarkaka gaba ɗaya, ka kuma biya musu kome don su samu su yi aski.
Ta haka kowa zai sani babu gaskiya a waɗannan rahotanni game da kai, za a kuma
ga cewa kai kanka kana kiyaye dokar. 25 Game da Alʼummai masu bi kuwa, mun yi
musu wasiƙa a kan shawararmu cewa su guji abincin da aka miƙa wa gumaka, da
jini, da naman dabbar da aka maƙure da kuma fasikanci."
26 Kashegari, sai Bulus ya ɗauki mutanen ya kuma tsarkake kansa tare da su. Saʼan
nan ya tafi haikali domin yă sanar da ranar cikar tsarkakewarsu da kuma ranar da
za a ba da sadaka domin kowannensu.

### *An kama Bulus*

27 Da kwana bakwai ɗin suka yi kusan cika, waɗansu Yahudawa daga lardin Asiya
suka ga Bulus a haikali. Sai suka zuga taron duka, suka kama shi, 28 suna ihu suna
cewa "Mutanen Israʼila ku taimake mu! Ga mutumin da yake koya wa dukan mutane
koʼina cewa su ƙi mutanenmu da dokarmu da kuma wannan wuri. Ban da haka ma,
ya kawo Hellenawa a cikin filin haikali ya ƙazantar da wurin nan mai tsarki." 29 (Dā
ma can sun ga Turofimus mutumin Afisa a birni tare da Bulus suka yi tsammani
Bulus ya kawo shi filin haikali.)
30 Duk birnin ya ruɗe, mutane suka zaburo da gudu daga kowane gefe. Suka
kama Bulus, suka ja shi daga haikali, nan da nan aka rurrufe ƙofofi. 31 Yayinda
suke ƙoƙari su kashe shi, sai labari ya kai ga shugaban ƙungiyar sojan Roma cewa
birnin Urushalima duk ta hargitse. 32 Nan da nan ya ɗibi waɗansu hafsoshi da sojoji

suka gangara a guje wurin taron. Da masu hargitsin suka ga shugaban ƙungiyar
sojan da sojojinsa, sai suka daina dūkan Bulus.
33 Shugaban ƙungiyar sojan ya zo ya kama shi ya ba da umarni a daure shi da
sarƙoƙi biyu. Sa'an nan ya yi tambaya ko shi wane ne, da kuma abin da ya yi.
34 Waɗansu daga cikin taron suka ɗau kururuwa suna ce abu kaza, waɗansu kuma
suna ce abu kaza, da yake shugaban ƙungiyar sojan ya kāsa samun ainihin tushen
maganar saboda yawan hayaniyar, sai ya yi umarni a kai Bulus barikin soja. 35 Sa'ad
da Bulus ya kai bakin matakala, sai da sojoji suka ɗaga shi sama saboda tsananin
haukan taron. 36 Taron da suka bi suka dinga kururuwa, suna cewa, "A yi da shi!"

*Bulus ya yi wa taron jawabi*

37 Da sojoji suka kai gab da shigar da Bulus cikin bariki, sai ya ce wa shugaban
ƙungiyar sojan, "Ko ka yarda in yi magana da kai?"
Sai ya amsa ya ce, "Ka iya Girik ne? 38 Ba kai ba ne mutumin Masar nan da ya
haddasa tawaye har ya yi jagorar 'yan ta'ada dubu huɗu zuwa hamada a shekarun
baya?"
39 Bulus ya amsa ya ce, "Ni mutumin Yahuda ne, daga Tarshish a Silisiya
shahararren birnin nan. In ka yarda bari in yi wa mutane magana."
40 Da ya sami izini daga shugaban ƙungiyar sojan, sai Bulus ya tsaya a matakala,
ya ɗaga wa taron hannu. Da dukan suka yi shiru, sai ya ce musu da Arameyanci*,

# 22

1 "'Yan'uwa da iyaye, ku saurari kāriyata yanzu."
2 Da suka ji ya yi musu magana da Arameyik, sai suka yi tsit.
Sai Bulus ya ce, 3 "Ni mutumin Yahuda ne haifaffen Tarshish na Silisiya, amma
a nan birnin ne aka rene ni. Aka horar da ni sosai cikin dokokin kakanninmu a
ƙarƙashin Gamaliyel ni ma dā mai himma ne cikin bauta wa Allah kamar yadda
kowannenku yake a yau. 4 Na tsananta wa masu bin wannan Hanyar har ga
mutuwarsu, ina kama maza da mata ina kuma jefa su cikin kurkuku, 5 kamar yadda
babban firist da dukan Majalisa za su iya shaida. Na ma karɓi wasiƙu daga gare su
zuwa ga 'yan'uwansu a Damaskus, na kuma tafi can don in kawo waɗannan mutane
a daure zuwa Urushalima don a hukunta su.
6 "Wajen tsakar rana da na yi kusa da Damaskus, ba zato ba tsammani sai wani
babban haske daga sama ya haskaka kewaye da ni. 7 Sai na fāɗi a ƙasa na kuma ji
wata murya ta ce mini, 'Shawulu! Shawulu! Don me kake tsananta mini?'
8 "Sai na yi tambaya na ce, 'Wane ne kai, ya Ubangiji?'
"Ya amsa ya ce, 'Ni ne Yesu Banazare, wanda kake tsanantawa.' 9 Abokan tafiyata
suka ga hasken, amma ba su fahimci muryar mai magana da ni ba.
10 "Sai na yi tambaya, na ce, 'Me zan yi, ya Ubangiji?'
"Ubangiji ya ce, 'Tashi, ka tafi cikin Damaskus. A can za a faɗa maka duk abin da
aka shirya za ka yi.' 11 Abokan tafiyata suka ja ni a hannu zuwa cikin Damaskus,
saboda ƙarfin hasken ya makanta ni.
12 "Wani mutumin da ake kira Ananiyas ya zo ya gan ni. Shi mai ibada ne wajen
kiyaye dokoki wanda dukan Yahudawan da suke zama a can suna girmama shi
ƙwarai. 13 Ya tsaya kusa da ni ya ce, 'Dan'uwa Shawulu, ka sami ganin garinka!'
A daidai lokacin kuwa na iya ganinsa.
14 "Sa'an nan ya ce, 'Allah na kakanninmu ya zaɓe ka ka san nufinsa ka kuma ga
Mai Adalcin nan ka kuma ji kalmomi daga bakinsa. 15 Za ka zama mai shaidarsa ga

* **21:40** Ko kuwa mai yiwuwa Da Ibraniyanci haka ma a Mat 22.2

dukan mutane game da abin da ka gani ka kuma ji. [16] Yanzu me kake jira? Ka tashi,
a yi maka baftisma, a wanke zunubanka, ta wurin kira bisa ga sunansa.'
[17] "Sa'ad da na dawo Urushalima ina cikin addu'a a haikali, sai na ga wahayi [18] na
ga Ubangiji yana magana. Ya ce mini, 'Maza! Ka bar Urushalima, gama ba za su
yarda da shaidarka game da ni ba.'
[19] "Na amsa na ce, 'Ubangiji, waɗannan mutane sun san cewa na bi majami'a-
majami'a na jefa waɗanda suka gaskata da kai a cikin kurkuku, in kuma yin musu
dūka. [20] Sa'ad da kuma aka zub da jinin Istifanus mashaidinka, na tsaya can ina ba
da goyon bayana ina kuma tsaron tufafin masu kisansa.'
[21] "Sa'an nan Ubangiji ya ce mini, 'Je ka; zan aike ka can nesa a wurin Al'ummai.' "

*Bulus ɗan ƙasar Roma*

[22] Taron suka saurari Bulus sai da ya yi wannan magana. Sa'an nan suka ɗaga
muryoyinsu suka yi ihu suka ce, "A raba duniya da wannan mutum! Bai cancanci yă
rayu ba!"
[23] Da suna ihu suna kaɗa mayafansu suna da tā da ƙura sama, [24] sai shugaban
ƙungiyar sojan ya umarta a kai Bulus a barikin soja. Ya ba da umarni a yi masa bulala
a kuma tambaye shi abin da ya sa mutane suke masa ihu haka. [25] Suna kwantar da
shi ke nan domin a yi masa bulala, sai Bulus ya ce wa jarumin da yake tsaye a nan,
"Ashe, daidai ne bisa ga doka a yi wa ɗan ƙasar Roma bulala wanda ba a ma tabbatar
da laifi a kansa ba?"
[26] Da jarumin ya ji haka sai ya je wurin shugaban ƙungiyar sojan ya ce masa, "Me
kake so yi ne? Wannan mutum ɗan ƙasar Roma ne."
[27] Sai shugaban ƙungiyar sojan ya je ya tambayi Bulus ya ce, "Faɗa mini, kai ɗan
ƙasar Roma ne?"
Bulus ya ce, "I."
[28] Sai shugaban ƙungiyar sojan ya ce, "Sai da na biya kuɗi mai yawa kafin in zama
ɗan ƙasa."
Bulus ya ce, "Ni kuwa an haife ni ɗan ƙasa."
[29] Waɗanda dā suke shirin yin masa tambayoyi suka ja da baya nan da nan.
Shugaban ƙungiyar sojan kansa ya tsorata da ya fahimci cewa ya sa wa Bulus, ɗan
ƙasar Roma sarƙa.

*A gaban majalisa*

[30] Kashegari da yake shugaban ƙungiyar sojan ya so yă tabbatar da ainihin abin da
ya sa Yahudawa suke zargin Bulus, sai ya sake shi ya kuwa umarci manyan firistoci
da dukan Majalisar su taru. Sa'an nan ya kawo Bulus ya sa ya tsaya a gabansu.

# 23

[1] Bulus ya zuba wa Majalisar ido ya ce, "'Yan'uwana, na cika aikina ga Allah cikin
lamiri mai kyau har yă zuwa yau." [2] Da jin wannan Ananiyas babban firist ya umarci
waɗanda suke tsaye kusa da Bulus su buge bakinsa. [3] Sai Bulus ya ce masa, "Allah
zai buge ka, kai farin bango! Ka zauna a can kana hukunta ni bisa ga doka, ga shi
kai kanka kana ƙetare dokar ta wurin ba da umarni a buge ni!"
[4] Waɗanda suke tsaye kusa da Bulus kuwa suka ce masa, "Babban firist na Allah
za ka zaga?"
[5] Bulus ya amsa ya ce, "'Yan'uwa, ai, ban san cewa shi ne babban firist ba; gama
yana a rubuce cewa, 'Kada ka yi mugun magana game da mai mulkin mutanenka.'*"
[6] Bulus, da ya gane cewa waɗansu daga cikinsu Sadukiyawa ne sauran kuma
Farisiyawa ne, sai ya ɗaga murya a Majalisar ya ce, "'Yan'uwana, ni Bafarisiye ne,
ɗan Farisiyawa. Ana mini shari'a saboda begen da nake da shi a kan tashin matattu."

* **23:5** Fit 22.28

7 Da ya faɗi haka, sai gardama ta tashi tsakanin Farisiyawa da Sadukiyawa, taron
kuwa ya rabu biyu. 8 (Sadukiyawa suna cewa babu tashin matattu, babu mala'iku ko
ruhohi. Amma Farisiyawa kuwa sun tsaya a kan cewa duk akwai.)
9 Aka yi babbar hayaniya. Waɗansu daga cikin malaman dokokin da suke
Farisiyawa suka miƙe tsaye suka yi gardama mai ƙarfi suna cewa, "Ba mu sami wani
laifi a wurin mutumin nan ba. A ce wani ruhu ko mala'ika ne ya yi masa magana
fa?" 10 Gardamar kuwa ta yi tsanani har shugaban ƙungiyar sojan ya ji tsoro za su
yayyage Bulus. Ya umarci sojoji su tafi su ƙwace shi ƙarfi da yaji daga wurinsu su
kawo shi cikin barikin soja.
11 Kashegari da dare Ubangiji ya tsaya kusa da Bulus ya ce, "Ka yi ƙarfin hali! Don
kamar yadda ka yi shaida game da ni a Urushalima, haka kuma lalle, za ka yi shaidata
a Roma."

### *Kulla shawara don a kashe Bulus*

12 Kashegari, Yahudawa suka ƙulla makirci suka kuma yi rantsuwa cewa ba za su
ci ko sha ba sai sun kashe Bulus. 13 Fiye da mutane arba'in ne suka ƙulla wannan
makirci. 14 Suka je wajen manyan firistoci da dattawa suka ce, "Mun yi babbar
rantsuwa cewa ba za mu ci kome ba sai mun kashe Bulus. 15 Saboda haka, sai ku da
Majalisa sai ku roƙi shugaban ƙungiyar sojan yǎ kawo shi a gabanku kamar kuna
so ku ƙara samun cikakken bayani game da zancensa. Mu kuwa muna a shirye mu
kashe shi kafin yǎ iso nan."
16 Amma da ɗan 'yar'uwar Bulus ya ji wannan makirci, sai ya tafi cikin barikin
soja ya gaya wa Bulus.
17 Sai Bulus ya kira ɗaya daga cikin jarumawan ya ce, "Ka kai wannan saurayi
wurin shugaban ƙungiyar soja; yana da wani abin da zai faɗa masa." 18 Saboda
haka ya ɗauke shi ya kai wajen shugaban ƙungiyar sojan.
Jarumin ya ce, "Bulus, ɗan kurkukun nan ya kira ni, ya roƙe ni in kawo wannan
saurayi a wurinka domin yana da wani abin da zai faɗa maka."
19 Sai shugaban ƙungiyar sojan ya kama hannun saurayin ya ja shi gefe, ya tambaye
shi cewa, "Mene ne kake so ka gaya mini?"
20 Saurayin ya ce, "Yahudawa sun ƙulla za su roƙe ka ka kawo Bulus a gaban
Majalisa gobe kamar suna neman ƙarin cikakken bayani game da Bulus. 21 Kada
ka yarda da su, domin fiye da mutum arba'in daga cikinsu suna fakonsa. Sun yi
rantsuwa ba za su ci ko sha ba sai sun kashe shi. Suna nan a shirye yanzu, suna jira
ka amince da roƙonsu."
22 Sai shugaban ƙungiyar sojan ya sallami saurayin ya kwaɓe shi ya ce, "Kada ka
gaya wa kowa cewa ka faɗa mini wannan."

### *An tura Bulus zuwa Kaisariya*

23 Sai ya kira biyu daga cikin jarumawansa, ya umarce su cewa, "Ku shirya sojoji
ɗari biyu, da masu hawan dawakai saba'in da kuma masu māsu ɗari biyu su tafi
Kaisariya da ƙarfe tara na daren nan. 24 Ku shirya wa Bulus dawakai da zai hau don
a kai shi wurin Gwamna Felis lafiya."
25 Ya kuma rubuta wasiƙa kamar haka,
26 Kalaudiyus Lisiyas.
Zuwa ga Mai Girma, Gwamna Felis.
Gaisuwa.
27 Yahudawa sun kama wannan mutum suna kuma dab da kashe shi, amma na
zo da sojojina na ƙwato shi, saboda na ji shi ɗan ƙasar Roma ne. 28 Na so in san
abin da ya sa suke zarginsa, saboda haka na kawo shi a gaban Majalisarsu. 29 Na
tarar cewa zargin da ake masa ya shafi waɗansu abubuwan da suka shafi dokarsu
ne, amma ba wani zargi a kansa da ya isa kisa ko a daure shi. 30 Sa'ad da na sami

labari cewa akwai wani makircin da aka ƙulla masa, sai na aika shi wurinka nan
da nan. Na kuma umarci masu zarginsa su kai ƙararsu gare ka.
31 Saboda haka sojojin, don cika umarni, suka ɗauki Bulus da dad dare suka kawo
shi har Antifatiris. 32 Kashegari suka bar masu hawan dawakai suka ci gaba da shi,
yayinda sojojin suka koma barikin soja. 33 Sa'ad da masu hawan dawakai suka isa
Kaisariya, sai suka ba wa gwamna wasiƙar suka kuma miƙa masa Bulus. 34 Gwamna
ya karanta wasiƙar ya kuma tambaya ko daga wanda lardi ne ya fito. Da ya ji cewa
shi daga Silisiya ne, 35 sai ya ce, "Zan ji batunka lokacin da masu zarginka suka iso."
Sa'an nan ya ba da umarni a kai Bulus a tsare shi a fadar Hiridus.

# 24

*Shari'a a gaban Felis*

1 Bayan kwana biyar sai Ananiyas babban firist ya tafi Kaisariya tare da waɗansu
daga cikin dattawa da kuma wani lauya mai suna Tertullus, suka kawo ƙararsu game
da Bulus a gaban gwamna. 2 Sa'ad da aka shigo da Bulus, sai Tertullus ya shiga kai
ƙararsa a gaban Felis yana cewa, "Mun daɗe muna zaman lafiya a ƙarƙashinka,
hangen nesanka kuma ya kawo gyare-gyare a wannan ƙasa. 3 Ko'ina da kuma a
kowace hanya, ya mafifici Felis, mun amince da wannan da godiya marar iyaka.
4 Amma don kada in ƙara gajiyar da kai, ina roƙonka ka yi haƙuri ka saurari ɗan
taƙaitaccen jawabinmu.
5 "Mun tarar da wannan mutum fitinanne ne, yana tā-da-na-zaune-tsaye a
tsakanin Yahudawa ko'ina a duniya. Shi shugaban ɗarikar Nazarawa 6 har ma ya
yi ƙoƙari ya ƙazantar da haikali; shi ya sa muka kama shi.* 8 Ta wurin bincika shi
da kanka za ka gane gaskiyar game da dukan waɗannan zargin da muke kawo a
kansa."
9 Yahudawa ma suka goyi bayan zargin, suna tabbatar cewa waɗannan abubuwa
haka suke.
10 Da gwamna ya yi masa alama yă yi magana, sai Bulus ya amsa ya ce, "Na san
cewa ka yi shekaru da yawa kana mulki a wannan ƙasa; saboda haka ina farin ciki in
kāre kaina. 11 Da sauƙi za ka iya tabbatar cewa, bai fi kwana goma sha biyu da suka
wuce ne na tafi Urushalima, domin yin sujada ba. 12 Masu zargina ba su same ni ina
gardama da kowa a haikali, ko kuma ina tā da hankalin jama'a a majami'u ko kuwa
wani wuri dabam a cikin birni ba. 13 Ba kuwa za su iya tabbatar maka ƙarar da suke
yi yanzu a kaina ba. 14 Amma na yarda cewa ina bauta wa Allah na kakanninmu a
matsayin mai bin Hanyar da suke kira ɗarika. Na gaskata dukan abin da ya amince
da Doka da yake kuma a rubuce cikin Annabawa, 15 ina kuma da irin bege ɗaya ga
Allah yadda mutanen nan suke da shi, cewa akwai tashin matattu masu adalci da
masu mugunta duka. 16 Saboda haka, ina ƙoƙari kullum in kasance da lamiri mai
tsabta a gaban Allah da mutane.
17 "Bayan 'yan shekaru da dama da ba na nan, sai na dawo Urushalima don in kawo
wa mutanena kyautai saboda matalauta in kuma yi sadaka. 18 Ni tsarkake ne sa'ad
da suka same ni cikin filin haikalin ina yin haka. Babu taro tare da ni, ba kuwa ina
tā da hankali ba. 19 Amma akwai waɗansu Yahudawa daga lardin Asiya, waɗanda
ya kamata suna a nan a gabanka su kawo ƙara in suna da wani a kaina. 20 Ko kuwa
waɗannan da suke a nan su faɗi laifin da suka same ni da shi sa'ad da na tsaya a
gaban Majalisa, 21 sai ko wannan abu ɗaya kaɗai da na ɗaga murya na faɗi yayinda

---

* **24:6** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da shi, sun kuwa so su hukunta shi bisa ga doka. 7 Amma shugaban, Lisiyas, ya zo ya ɗauke shi daga hannunmu ƙarfi da yaji, 8 yana kuma umarci masu zarginsa su zo gabanka

nake tsaye a gabansu cewa, ‘A game da tashin matattu ake mini shari’a a gabanku yau.’ ”
22 Sai Felis, wanda yake da cikakken sani game da Hanyar, ya ɗaga sauraron ƙarar.
Ya ce, “In Lisiyas shugaban ƙungiyar soja ya iso, zan yanke muku shari’a.” 23 Ya yi
wa jarumin umarni yǎ tsare Bulus amma yǎ ba shi ’yanci yǎ kuma bar abokansa su
lura da bukatunsa.
24 Bayan ’yan kwanaki da dama sai Felis ya zo da matarsa Durusilla, mutuniyar
Yahuda. Sai ya aika a zo da Bulus ya kuma saurare shi da yake magana game da
bangaskiya cikin Kiristi Yesu. 25 Da Bulus ya ci gaba jawabi a kan adalci, kamunkai
da kuma hukunci mai zuwa, sai Felis ya tsorata ya ce, “Yanzu kam, ya isa haka! Kana
iya tafi. In na sami zarafi, zan kira ka.” 26 A wani fanni yana sa rai cewa Bulus zai ba
shi toshiyar baki, saboda haka ya yi ta aika a kira masa Bulus yǎ yi magana da shi.
27 Da shekaru biyu suka wuce, sai Forsiyus Festus, ya gāji Felis, amma domin Felis
ya so yǎ biya wa Yahudawa bukata, sai ya bar Bulus a kurkuku.

# 25

### *Shari’a a gaban Festus*

1 Kwana uku bayan isowa a lardin, sai Festus ya haura daga Kaisariya zuwa
Urushalima, 2 inda manyan firistoci da shugabannin Yahudawa suka bayyana a
gabansa suka kuma gabatar da ƙararsu a kan Bulus. 3 Suka roƙi Festus a gaggauce a
matsayin alfarma gare su, da yǎ sa a mai da Bulus Urushalima, gama sun ’yan kwanto
su kashe shi a hanya. 4 Festus ya amsa ya ce, “Bulus yana tsare a Kaisariya, ni da
kaina kuma zan je can ba da daɗewa ba. 5 Ku sa waɗansu daga cikin shugabanninku
su tafi tare da ni su kawo ƙararsu a kan mutumin a can, in ya aikata wani laifi.”
6 Bayan ya yi kwanaki takwas ko goma tare da su, sai ya gangara zuwa Kaisariya,
kashegari kuma ya kira a yi zaman kotu ya kuma umarta a kawo Bulus a gabansa.
7 Da Bulus ya bayyana, sai Yahudawan da suka gangaro daga Urushalima suka tsaya
kewaye shi, suna kawo ƙarar masu tsanani da yawa a kansa, waɗanda ba su iya
tabbatarwa ba.
8 Sa’an nan Bulus ya kāre kansa ya ce, “Ban aikata wani laifi game da dokokin
Yahudawa ko game da haikali ko kuma game da Kaisar ba.”
9 Festus, da yake yana so yǎ yi wa Yahudawa alfarma, sai ya ce wa Bulus, “Ka yarda
ka je Urushalima a yi maka shari’a a can a gabana a kan waɗannan zarge?”
10 Bulus ya amsa ya ce, “Yanzu ina tsaye a gaban kotun Kaisar, inda ya kamata a
yi mini shari’a. Ban yi wani laifi ga Yahudawa ba, kai da kanka ma ka san da haka
sarai. 11 In kuwa ina da wani laifin da ya isa kisa, ban ƙi in mutu ba. Amma in ƙarar
da waɗannan Yahudawa suka kawo a kaina ba gaskiya ba ne, ba wanda yake da iko
ya ba da ni a gare su. Na ɗaukaka ƙara zuwa gaban Kaisar!”
12 Bayan Festus ya yi shawara da majalisarsa sai ya ce, “Ka ɗaukaka ƙara zuwa
gaban Kaisar. To, ga Kaisar kuwa za ka tafi!”

### *Festus ya nemi shawarar Sarki Agiriffa*

13 Bayan ’yan kwanaki sai Sarki Agiriffa da Bernis suka iso Kaisariya don su yi wa
Festus gaisuwar bangirma. 14 Da yake za su yi kwanaki da dama a can, sai Festus
ya tattauna batun Bulus da sarki. Ya ce, “Akwai mutumin da Felis ya bari a daure.
15 Sa’ad da na je Urushalima, manyan firistoci da dattawan Yahudawa suka kawo
ƙara game da shi suka kuma nema a hukunta shi.
16 “Na gaya musu cewa ba al’adar Romawa ba ce a hukunta mutum kafin ya
fuskanci masu ƙararsa ya kuma sami damar kāre kansa game da ƙararsu. 17 Da
suka zo nan tare da ni, ban yi wani jinkiri ba, na kira zaman kotu kashegari kuma

na umarta a kawo mutumin. 18 Sa'ad da masu zarginsa suka tashi tsaye don su yi
magana, ba su zarge shi da wani laifin da na yi tsammani ba. 19 A maimako haka,
sai suka kawo waɗansu 'yan maganganu game da addininsu da ba su yarda da shi
ba da kuma game da wani Yesu da ya mutu wanda Bulus ya ce yana da rai. 20 Na
rasa yadda zan bincike irin abubuwan nan; saboda haka na yi tambaya ko zai yarda
ya tafi Urushalima a yi masa shari'a a can game da waɗannan zargi. 21 Da Bulus ya
ɗaukaka ƙara zuwa gaban Babban Sarki sai na umarta a tsare shi har kafin in aika
shi zuwa ga Kaisar."

22 Sai Agiriffa ya ce wa Festus, "Ni ma zan so in saurari mutumin da kaina."

Sai ya amsa ya ce, "Za ka kuwa ji shi gobe."

### *Bulus a gaban Agiriffa*

23 Kashegari Agiriffa da Bernis suka yi shiga irin ta sarauta suka shiga ɗakin jama'a
tare da manyan sojoji da manyan mutanen birni. Da umarnin Festus, sai aka shigo
da Bulus. 24 Sai Festus ya ce, "Sarki Agiriffa, da kuma dukan waɗanda suke tare
da mu, kun ga wannan mutum! Dukan jama'ar Yahudawa sun kawo mini kararsa
a Urushalima da kuma a nan Kaisariya, suna kururuwa suna cewa bai kamata a
bar shi da rai ba. 25 Ban same shi da wani laifin da ya isa kisa ba, amma saboda
ya ɗaukaka ƙararsa zuwa gaban Babban Sarki sai na yanke shawara in aika da shi
Roma. 26 Ba ni da wata tabbatacciyar maganar da zan rubuta wa Mai Girma game da
shi. Saboda haka na kawo shi a gabanku duka, musamman a gabanka, Sarki Agiriffa,
saboda a sakamakon wannan bincike zan iya samun abin da zan rubuta. 27 Don a
ganina wauta ce a aika da ɗan kurkuku ba tare da an nuna zargin da ake yi a kansa
ba."

## 26

1 Sai Agiriffa ya ce wa Bulus, "An ba ka izini ka yi magana."

Saboda haka Bulus ya yi alama da hannunsa ya fara kāriyarsa. 2 Ya ce, "Sarki
Agiriffa, na yi sa'a da na tsaya a gabanka yau yayinda nake kāriyata game da dukan
zargin Yahudawa, 3 musamman ma domin ka saba sosai da dukan al'adun Yahudawa
da kuma maganganunsu. Saboda haka ina roƙonka ka saurare ni da haƙuri.

4 "Yahudawa duk sun san yadda na yi rayuwa tun ina yaro, daga farkon rayuwata
a ƙasarmu da kuma a Urushalima. 5 Sun san ni tun da daɗewa za su kuwa shaida,
in suna so, cewa bisa ga ɗarikar addininmu mafi tsanani, na yi rayuwar Bafarisiye
ne. 6 Yanzu kuwa saboda begena cikin abin da Allah ya yi wa kakanninmu alkawari
ne, ake mini shari'a yau. 7 Wannan shi ne alkawarin da kabilanmu goma sha biyu
suke bege su ga cikawarsa, yayinda suke bauta wa Allah da himma dare da rana. Ya
Sarki, saboda wannan bege ne fa Yahudawa suke zargena. 8 Don me wani a cikinku
zai yi shakka cewa Allah yana tā da matattu?

9 "Ni ma a dā na tabbata cewa ya kamata in yi duk abin da zan iya yi domin in
yi gāba da sunan Yesu Banazare. 10 Abin da na yi ke nan a Urushalima. Da izinin
manyan firistoci na sa tsarkaka da yawa a kurkuku, sa'ad da kuma ake kashe su,
nakan ka da ƙuri'ata gāba da su. 11 Sau da dama nakan bi majami'a-majami'a, in sa
a yi musu hukunci. Na kuma yi ƙoƙarin tilasta su su yi saɓo. Don kuma tsananin
fushi da su, sai da na fafare su har waɗansu garuruwa na ƙetaren iyaka, ina tsananta
musu.

12 "A cikin irin tafiye-tafiyen nan ne ina kan hanya zuwa Damaskus tare da izini
daga manyan firistoci. 13 Da tsakar rana, ya sarki, sa'ad da nake kan hanya, sai na
ga wani haske daga sama, fiye da hasken rana, yana haskakawa kewaye da ni da
abokan tafiyata. 14 Dukanmu muka fāɗi ƙasa, na kuwa ji wata murya tana ce mini

da harshen Arameyik, ‘Shawulu, Shawulu, don me kake tsananta mini? Yana da
wuya ka shuri tsinken tsokanar dabba.’
15 “Sai na yi tambaya na ce, ‘Wane ne kai, ya Ubangiji?’
“Ubangiji ya ce, ‘Ni ne Yesu wanda kake tsananta wa. 16 Yanzu ka tashi, ka tsaya
da ƙafafunka. Na bayyana a gare ka don in naɗa ka bawa da kuma mai shaidar abin
da ka gani game da ni da kuma abin da zan nuna maka. 17 Zan tsirar da kai daga
mutanenka da kuma daga Al’ummai. Ina aikan ka zuwa gare su domin 18 ka buɗe
idanunsu su kuwa juyo daga duhu zuwa haske, daga mulkin Shaiɗan kuma zuwa
wurin Allah, domin su sami gafarar zunubai da kuma matsayi a cikin waɗanda aka
tsarkake ta wurin bangaskiya a cikina.’
19 “Saboda haka fa, Sarki Agiriffa, ban yi rashin biyayya ga wahayin nan daga
sama ba. 20 Da farko ga waɗanda suke a Damaskus, sa’an nan ga waɗanda suke a
Urushalima da kuma cikin dukan Yahudiya, da kuma ga Al’ummai su ma, na yi wa’azi
don su tuba su juyo ga Allah su kuma tabbatar da tubansu ta wurin ayyukansu. 21 Shi
ya sa Yahudawa suka kama ni a filin haikali suka kuma yi ƙoƙarin kashe ni. 22 Amma
na sami taimakon Allah har yă zuwa yau. Yanzu ga ni a tsaye a nan, ina shaida ga
babba da yaro. Ba na faɗin kome fiye da abin da annabawa da Musa suka ce zai
faru, 23 cewa Kiristi zai sha wahala, kuma a matsayin wanda yake na fari da zai tashi
daga matattu, zai yi shelar haske ga mutanensa da kuma Al’ummai.”
24 A nan ne fa Festus ya tsai da kāriyar Bulus. Ya yi ihu ya ce, “Bulus! Kai dai
ruɗaɗɗe ne, yawan karatunka yana juya maka kai.”
25 Bulus ya amsa ya ce, “Ba na hauka, ya mafifici Festus. Abin da nake faɗi gaskiya
ne da kuma mai kyau. 26 Sarki ya san waɗannan abubuwa, ina kuma iya yin magana
da shi a sake. Na tabbata cewa ba ɗaya daga cikin waɗannan da ya kuɓuce saninsa,
domin ba a ɓoye aka yi shi ba. 27 Sarki Agiriffa ka gaskata da annabawa? Na san ka
gaskata.”
28 Sai Agiriffa ya ce wa Bulus, “Kana tsammani cewa a cikin ɗan ƙanƙanin lokaci
kana so ka mai da ni Kirista?”
29 Bulus ya amsa ya ce, “Ko a ɗan lokaci, ko a lokaci mai yawa, ina addu’a ga Allah
cewa, ba kai kaɗai ba amma duk waɗanda suke saurare ni a yau su zama abin da
nake, sai dai ban da sarƙoƙin nan.”
30 Sai sarki ya tashi, haka kuma gwamna da Bernis da kuma waɗanda suke zaune
tare da su. 31 Suka bar ɗakin, kuma yayinda suke magana da juna, sai suka ce,
“Wannan mutum ba ya yin kome da ya isa kisa ko dauri.”
32 Sai Agiriffa ya ce wa Festus, “Da ba don wannan mutum ya ɗaukaka ƙara zuwa
gaban Kaisar ba da an sake shi.”

## 27

### *Bulus ya tafi Roma a jirgin ruwa*

1 Sa’ad da aka yanke shawara cewa za mu tashi a jirgin ruwa zuwa Italiya, sai aka
danƙa Bulus da waɗansu ’yan kurkuku a hannun wani jarumin mai suna Juliyos,
wanda yake na Bataliyar Babban Sarki. 2 Muka shiga jirgin ruwa daga Andiramitiyum
wanda yake shirin tashi zuwa tasoshin da suke bakin tekun lardin Asiya, sai muka
kama tafiya. Aristarkus, mutumin Makidoniya daga Tessalonika, yana tare da mu.
3 Kashegari muka sauka a Sidon; Juliyos kuwa, cikin alheri ga Bulus, ya bar shi yă je
wajen abokansa domin su biya masa bukatunsa. 4 Daga can kuma muka sāke kama
tafiya muka zaga ta bayan tsibirin Saifurus saboda iska tana gāba da mu. 5 Sa’ad
da muka ƙetare tekun da yake sassan gaɓar Silisiya da Famfiliya sai muka sauka a
Mira ta Lisiya. 6 A can jarumin ya sami wani jirgin ruwan Alekzandariyan da za shi
Italiya sai ya sa mu a ciki. 7 Tafiyar ta ɗauki kwanaki da yawa muna yi kaɗan-kaɗan

da ƙyar muka iso kusa da gaɓar Kinidus. Da iskar ta hana mu ci gaba, sai muka bi
ta bayan tsibirin Kirit ɗaura da Salmone. 8 Muka ci gaba a gefen gaɓar da ƙyar har
muka iso wani wurin da ake kira Kyakkyawan Mafaka, kusa da garin Laseya.
9 An riga an ɓata lokaci da yawa, tafiya kuwa ta riga ta zama da hatsari domin a
lokacin Azumi* ya riga ta wuce. Saboda haka Bulus ya gargaɗe su, 10 ya ce, "Mutane,
ina gani tafiyarmu za tă zama da masifa ta kuma kawo babbar hasara ga jirgin ruwan
da kaya, da kuma ga rayukanmu ma." 11 Amma jarumin, a maimakon ya saurari
abin da Bulus ya ce, sai ya bi shawarar matuƙi da kuma mai jirgin ruwan. 12 Da yake
tashar jirgin ruwan ba tă dace a ci damina a can ba, yawanci suka ba yanke shawara
cewa mu ci gaba da tafiya, da bege za mu kai Funis mu ci damina a can. Wannan
tashar jirgin ruwa ne a Kirit, tana fuskantar kudu maso yamma da kuma arewa maso
yamma.

### *Hadari*

13 Da iska ta fara busowa daga kudu a hankali, sai suka yi tsammani sun sami abin
da suke nema; saboda haka suka janye ƙugiyar jirgin ruwa suka bi ta gefen tsibirin
Kirit. 14 Ba a jima ba, sai ga wata guguwar iska mai ƙarfin da ake kira "'Yar arewa
maso gabas," ta buga daga tsibirin. 15 Iskar ta ci ƙarfin jirgin ruwan har ya kāsa
fuskantar iskar; saboda haka muka sallamar mata tă yi ta tura mu. 16 Da muka bi ta
bayan wani ɗan tsibirin da ake kira Kauda, da ƙyar muka jawo ɗan ƙaramin jirgin
kusa da jirgin. 17 Da mutanen suka jawo shi cikin babban jirgin ruwan, sai suka sa
igiyoyi ta ƙarƙashin jirgin ruwan kanta don su ɗaɗɗaura shi. Don gudun kada a
fyaɗa mu da yashin gaɓar Sirtis, sai suka saukar da ƙugiyar jirgin ruwan, suka bari
aka yi ta tura jirgin haka. 18 Haka muka yi ta shan bugun guguwar hadarin nan
kashegari suka fara jajjefar da kayan da jirgin yake ɗauke da su a cikin teku. 19 A
rana ta uku, da hannuwansu suka jefar da kayan aikin jirgin ruwan a cikin teku.
20 Da dai aka yi kwana da kwanaki ba a ga rana ko taurari ba guguwar iska kuma ta
ci gaba da bugowa, a ƙarshe muka fid da zuciya za mu tsira.
21 Bayan mutanen sun daɗe ba su ci abinci ba, Bulus ya miƙe tsaye a gabansu ya
ce, "Mutane, da kun ji shawarata na kada ku tashi daga Kirit, da ba ku fāɗa wannan
masifa da hasara ba. 22 Amma yanzu ina ƙarfafa ku ku yi ƙarfin hali, domin ba
ɗayanku da zai rasa ransa; jirgin ruwan ne kaɗai zai hallaka. 23 Jiya da dare wani
mala'ikan Allahn da nake nasa nake kuma bauta wa ya tsaya kusa da ni 24 ya ce,
'Kada ka ji tsoro, Bulus. Lalle za ka tsaya a gaban Kaisar a yi maka shari'a; Allah
kuma cikin alherinsa ya ba ka dukan rayukan mutanen da suke tafiya tare da kai.'
25 Saboda haka ku yi ƙarfin hali, ku jama'a, gama gaskata Allah a kan cewa yadda
aka faɗa mini ɗin nan, haka zai faru. 26 Duk da haka, dole a fyaɗa mu a wani tsibiri."

### *Jirgin ruwa ya yi hatsari*

27 A dare na goma sha huɗu iska dai tana ta korarmu a Tekun Adiriyatik, wajen
tsakar dare sai masu tuƙin jirgin suka zaci sun yi kusa da ƙasa. 28 Sai suka gwada
zurfin ruwan suka ga ya kai ƙafa ɗari da ashirin. Bayan ɗan lokaci kaɗan suka sāke
gwadawa suka ga zurfin ya kai ƙafa tasa'in. 29 Don gudun kada a fyaɗa mu a kan
duwatsu, sai suka saki ƙugiyoyin jirgin guda huɗu daga bayan jirgin suka yi fata gari
ya waye. 30 Cikin ƙoƙarin tserewa daga jirgin, sai masu tuƙin jirgin suka saukar da
ɗan ƙaramin jirgin ruwan cikin tekun, suka yi kamar za su saki waɗansu ƙugiyoyi
daga sashen gaba na babban jirgin ne. 31 Sai Bulus ya ce wa jarumin da kuma sojojin,
"In mutanen nan ba su tsaya a cikin jirgin nan ba, ba za ku tsira ba." 32 Sai sojojin
suka yayyanke igiyoyin da suke riƙe da ɗan ƙaramin jirgin, suka bar shi ya bi ruwa.

* **27:9** Wato, da Ibraniyanci Ranar Kafara ke nan (Yom Kippur)

[33] Kafin gari ya waye Bulus ya roƙe su duka su ci abinci. Ya ce, "Kwana goma sha
huɗu ke nan, kuna zama cikin zulumi kun kuma kasance ba abinci, ba ku ci kome
ba. [34] Ina roƙonku yanzu ku ci abinci. Kuna bukatarsa don ku rayu. Ba ɗayanku da
zai rasa ko gashin kansa guda ɗaya." [35] Bayan da ya faɗi haka, sai ya ɗauki burodi
ya yi godiya ga Allah a gabansu duka. Sa'an nan ya gutsuttsura ya fara ci. [36] Dukansu
kuwa suka sami ƙarfafawa, suka kuma ci abinci. [37] Dukanmu a jirgin kuwa mutane
276 ne. [38] Sa'ad da suka ci iyakar abin da suke so, sai suka rage nauyin jirgin ta wurin
zubar da hatsin a cikin tekun.
[39] Da gari ya waye, ba su gane ƙasar da suke ba, amma suka ga wani lungu da gaci
mai yashi, sai suka yanke shawara su kai jirgin can in za su iya. [40] Da suka yanke
ƙugiyoyin, sai suka bar su a cikin teku a lokaci guda kuma suka ɓalle maɗaurin abin
juya jirgin. Sai suka tā da filafilan gaban jirgin daidai yadda iska za tă tura shi gaba,
sa'an nan suka nufi gaci. [41] Amma jirgin ruwan ya shiga yashi ya kafe. Kan jirgin ya
shiga cikin yashin ya kāsa motsi, sai jirgin ya fara farfashewa ta baya saboda haukan
raƙuman ruwa.
[42] Sojojin suka yi niyya su kakkashe 'yan kurkukun don hana waninsu yă yi iyo yă
tsere. [43] Amma jarumin ya so yă ceci ran Bulus, sai ya hana su aiwatar da niyyarsu.
Ya kuma yi umarni duk waɗanda suka iya ruwa su fara fāɗawa zuwa gaci. [44] Sauran
kuma su bi katakai zuwa can ko kuma a kan tarkacen jirgin ruwan. Ta haka kowa
ya kai bakin teku lafiya.

# 28

*Tsibirin Malta*

[1] Bayan da muka kai bakin tekun lafiya, sai muka tarar cewa sunan tsibirin Malta
ne. [2] Mutanen tsibirin kuwa suka nuna mana babban alheri. Suka hura wuta suka
marabce mu duka saboda ana ruwan sama da kuma sanyi. [3] Bulus ya tattara tarin
itace, yayinda kuma yake sa itacen a wuta, sai maciji ya ɓullo saboda zafi, ya dāfe a
hannunsa. [4] Da mutanen tsibirin suka ga macijin yana lilo a hannunsa, sai suka ce
wa juna "Lalle, wannan mutum mai kisankai ne; gama ko da yake ya tsira daga teku,
Adalci bai bar shi ya rayu ba." [5] Amma Bulus ya karkaɗe macijin a cikin wuta, bai
kuwa ji wani ciwo ba. [6] Mutanen kuma suka yi zato zai kumbura ko kuma nan da
nan zai fāɗi matacce, amma da aka daɗe ba su ga wani abu ya faru da shi ba, sai
suka sāke ra'ayi suka ce shi wani allah ne.
[7] Akwai wani filin nan kusa wanda yake na Fubiliyus, babban shugaban tsibirin. Shi
ne ya karɓe mu a gidansa da alheri ya kuma ciyar da mu har kwana uku. [8] Mahaifinsa
kuwa yana kwanciya a gado yana fama da zazzaɓi da atuni. Bulus ya shiga ciki don
yă gan shi, bayan ya yi masa addu'a, sai ya ɗibiya masa hannuwa ya warkar da shi.
[9] Sa'ad da wannan ya faru, sauran marasa lafiya a tsibirin suka zo aka kuma warkar
da su. [10] Suka girmama mu ta kowane hali da muka shirya za mu tashi, sai suka ba
mu abubuwan da muke bukata.

*Isowa a Roma*

[11] Bayan wata uku sai muka tashi a wani jirgin ruwan da ya ci damina a tsibirin.
Jirgin ruwa kuwa na Alekzandariya ne yana da siffar tagwayen allolin Kasto da Follus.
[12] Muka isa Sirakus a can muka yi kwana uku. [13] Daga can muka tashi muka isa
Regiyum. Kashegari iskar kudu ta taso, kashegari kuma muka kai Futeyoli. [14] A can
muka tarar da waɗansu 'yan'uwa waɗanda suka gayyaci mu mu yi mako ɗaya da su.
Da haka dai muka kai Roma. [15] 'Yan'uwan da suke can sun sami labari cewa muna
zuwa, sai suka tashi tun daga Kasuwar Affiyus da Masauƙi Uku don su tarye mu. Da
ganin mutanen nan sai Bulus ya gode wa Allah ya kuma sami ƙarfafawa. [16] Da muka
isa Roma, sai aka yarda wa Bulus yă zauna shi kaɗai, tare da sojan da zai yi gadinsa.

*Bulus ya yi wa'azi a Roma a tsare*

17 Bayan ƙwana uku sai ya kira taron shugabannin Yahudawa. Da suka taru, Bulus
ya ce musu, "'Yan'uwana, ko da yake ban yi wa mutanenmu wani laifi ba ko kuma
wani abu game da al'adun kakanninmu, aka kama ni a Urushalima aka kuma ba da
ni ga Romawa. 18 Suka tuhume ni suka kuma so su sake ni, domin ba a same ni da
wani laifin da ya cancanci kisa ba. 19 Amma da Yahudawa suka ƙi, sai ya zama mini
dole in ɗaukaka ƙara zuwa gaban Kaisar ba don ina da wani zargin da zan kawo
game da mutanena ba. 20 Saboda wannan ne na nemi in gan ku in kuma yi magana
da ku. Saboda begen Isra'ila ne, nake a daure da wannan sarƙa."

21 Suka amsa cewa, "Ba mu sami wani wasiƙa daga Yahudiya game da kai ba, kuma
ba kowa daga cikin 'yan'uwan da suka zo daga can ya kawo wani labari ko ya faɗi
wani mummuna abu game da kai. 22 Amma muna so mu ji ra'ayinka, gama mun san
cewa mutane ko'ina suna muguwar magana a kan wannan ɗarikar."

23 Suka shirya su sadu da Bulus wata rana, suka ma zo da yawa fiye da dā a wurin
da Bulus yake zama. Daga safe har zuwa yamma ya yi ta yin musu bayani, ya kuma
shaida musu mulkin Allah yana ƙoƙarin rinjayarsu game da Yesu daga Dokar Musa da
kuma daga Annabawa. 24 Waɗansu suka rinjayu da abin da ya faɗa, amma waɗansu
suka ba su gaskata ba. 25 Suka kāsa yarda da juna suka fara watsewa bayan Bulus ya
yi wannan magana guda cewa, "Ruhu Mai Tsarki ya faɗa wa kakannin-kakanninku
gaskiya sa'ad da ya ce ta bakin annabi Ishaya cewa,

26 " 'Je ka wurin mutanen nan ka ce,
"Za ku yi ta ji amma ba za ku fahimta ba;
za ku yi ta dubawa, amma ba za ku gani ba."
27 Gama zuciyar mutanen nan ta yi tauri;
da ƙyar suke ji da kunnuwansu,
sun kuma rufe idanunsu.
In ba haka ba za su iya gani da idanunsu,
su ji da kunnuwansu,
su fahimta a zukatansu,
su kuma juyo, in kuwa warkar da su.'*

28 "Saboda haka na so ku san cewa an aika da ceton Allah ga Al'ummai, za su kuwa
saurara!"†

30 Shekaru biyu cif Bulus ya zauna a can a gidansa na haya yana marabtar duk
wanda ya je wurinsa. 31 Ya yi wa'azin mulkin Allah yana kuma koyarwa game da
Ubangiji Yesu Kiristi, gabagadi ba tare da wani abu ya hana shi ba.

* **28:27** Ish 6.9,10 † **28:28** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da saurara! 29 Bayan ya faɗi haka, sai Yahudawa suka watse, suna gardama mai zafi a tsakaninsu

# Romawa

1 Bulus, bawan Kiristi Yesu, kirayaye don yă zama manzo, keɓaɓɓe kuma domin
bisharar Allah. 2 Bisharar da Allah ya yi alkawari tuntuni ta bakin annabawansa a
cikin Nassosi Masu Tsarki 3 game da Ɗansa. Wanda bisa ga mutuntakarsa, zuriyar
Dawuda ne. 4 Wanda bisa ga Ruhun tsarki, an shaida shi da iko cewa shi Ɗan Allah
ne ta wurin tashinsa daga matattu. Wannan bishara kuwa game da Yesu Kiristi
Ubangijinmu ne. 5 Ta wurinsa da kuma saboda sunansa, muka sami alheri muka
kuma zama manzanni don mu kira mutane daga cikin dukan Al'ummai zuwa ga
biyayyar da take zuwa daga bangaskiya. 6 Ku ma kuna cikin waɗanda aka kira ku
zama na Yesu Kiristi.

7 Wannan wasiƙa ce zuwa ga dukanku da kuke a Roma waɗanda Allah yake ƙauna,
waɗanda kuma ya kira domin su zama tsarkaka.

Alheri da salama daga Allah Ubanmu da kuma daga Ubangiji Yesu Kiristi, su
kasance tare da ku.

### *Bulus ya yi marmari yă ziyarci Roma*

8 Da farko, ina gode wa Allahna ta wurin Yesu Kiristi saboda ku duka, gama ana
ba da labarin bangaskiyarku a ko'ina a duniya. 9 Allah, wanda nake bauta wa da
dukan zuciyata cikin wa'azin bisharar Ɗansa, shi ne shaidata a kan yadda kullum
ina tunawa da ku 10 cikin addu'o'ina a kowane lokaci; ina kuma addu'a cewa a ƙarshe
in Allah ya yarda hanya za tă buɗe mini in zo wurinku.
11 Ina marmarin ganinku don in ba ku wata baiwar ruhaniya, don ku yi ƙarfi
12 wato, don ni da ku mu ƙarfafa juna ta wurin bangaskiyarmu. 13 Ina so ku sani
'yan'uwa cewa na yi shirin zuwa wurinku sau da dama (amma aka hana ni yin haka
sai yanzu). Na so in zo domin in sami mutane wa Kiristi a cikinku, kamar yadda na
yi a cikin sauran Al'ummai.
14 Ina da hakki ga Hellenawa da waɗanda ba Hellenawa ba, ga masu hikima da
kuma marasa azanci. 15 Shi ya sa na yi himma sosai in yi muku wa'azin bishara ku
ma da kuke a Roma.
16 Ba na jin kunyar bishara, gama ita ikon Allah ne domin ceton kowa da ya gaskata,
da farko ga Yahudawa, sa'an nan ga Al'ummai. 17 Gama a cikin bishara an bayyana
adalci daga Allah wanda yake ta wurin bangaskiya daga farko zuwa ƙarshe, kamar
yadda yake a rubuce cewa, "Mai adalci zai rayu ta wurin bangaskiya."*

### *Fushin Allah a kan 'yan adam*

18 Ana bayyana fushin Allah daga sama a kan dukan rashin sanin Allah da kuma
muguntar mutanen da suke danne gaskiya ta wurin muguntarsu, 19 gama abin da
ana iya sani game da Allah a bayyane yake a gare su, domin Allah ya bayyana musu
shi. 20 Gama tun halittar duniya halayen Allah marar ganuwa, madawwamin ikonsa
da kuma allahntakarsa, ana iya ganinsu sarai, ana fahimtarsu ta wurin abubuwan
da Allah ya halitta, domin kada mutane su sami wata hujja.
21 Gama ko da yake sun san Allah, ba su ɗaukaka shi a matsayin Allah ko su
gode masa ba, sai dai tunaninsu ya zama banza, zukatansu masu wauta kuma suka
duhunta. 22 Ko da yake sun ɗauka su masu hikima ne, sai suka zama wawaye, 23 suka

* **1:17** Hab 2.4

kuma yi musayar ɗaukakar Allah marar mutuwa da siffofin da aka ƙera su yi kama
da mutum mai mutuwa da tsuntsaye da dabbobi da kuma halittu masu ja da ciki.
24 Saboda haka Allah ya yashe su ga mugayen sha'awace-sha'awacen zukatansu ga
fasikanci don a ƙasƙantar da jikunansu ga yin abin kunya. 25 Sun sauya gaskiyar
Allah da ƙarya, suka kuma yi wa abubuwan da aka halitta sujada suna bauta musu
a maimakon Mahalicci, wanda ake yabo har abada. Amin.
26 Saboda wannan, Allah ya yashe su ga sha'awace-sha'awacensu masu banƙyama.
Har matansu suka sauya daga haɗuwar mace da miji wadda ita ce daidai bisa ga
halitta zuwa haɗuwa da 'yan'uwansu mata wadda ba daidai ba. 27 Haka ma maza
suka bar al'adar kwana da mata suka tunzura cikin sha'awar kwana da juna, abin
da ba daidai ba bisa ga halitta. Maza suka aikata rashin kunya da waɗansu maza,
suka jawo wa kansu sakamako daidai da bauɗewarsu.
28 Da yake ba su yi tunani cewa ya dace su riƙe sanin Allah da suke da shi ba, sai ya
yashe su ga tunanin banza da wofi, su aikata abin da bai kamata a yi ba. 29 Sun cika
da kowace irin ƙeta, mugunta, kwaɗayi, da tunanin banza da wofi. Suka kuma cika
da kishi, kisankai, faɗa, ruɗu, da kuma riƙo a zuci. Su masu gulma ne, 30 da masu
ɓata suna, masu ƙin Allah, masu rashin kunya, masu girman kai, masu rigima; sukan
ƙaga hanyoyin yin mugunta; suna rashin biyayya ga iyayensu; 31 su marasa hankali
ne, marasa bangaskiya, marasa ƙauna, marasa tausayi. 32 Ko da yake sun san dokar
adalcin Allah cewa masu aikata irin waɗannan abubuwa sun cancanci mutuwa, duk
da haka ba cin gaba da aikata waɗannan abubuwa kaɗai suke yi ba, har ma suna
goyon bayan masu yinsu.

# 2

*Shari'ar adalcin Allah*
1 Saboda haka, kai da kake ba wa wani laifi, ba ka da wata hujja, gama a duk lokacin
da kake ba wa wani laifi, kana hukunta kanka ne, domin kai da kake ba wa wani laifi
kai ma kana aikata waɗannan abubuwa. 2 Yanzu mun san cewa hukuncin Allah a
kan masu aikata waɗannan abubuwa daidai ne. 3 Saboda haka sa'ad da kai mutum
kurum, kana ba su laifi, duk da haka kana aikata abubuwan nan, kana tsammani za
ka tsere wa hukuncin Allah ne? 4 Ko kuma kana rena wadatar alherinsa, haƙurinsa,
da kuma jimrewarsa ne ba tare da sanin cewa alherin Allah yana kai ka ga tuba ba
ne?
5 Amma saboda taurinkanka da zuciyarka marar tuba, kana tara wa kanka fushi a
ranar fushin Allah, sa'ad da za a bayyana hukuncinsa mai adalci. 6 Allah, "Zai sāka
wa kowane mutum gwargwadon aikin da ya yi."* 7 Ga waɗanda ta wurin naciya
suna yin nagarta suna neman ɗaukaka, girma da rashin mutuwa, su za a ba su rai
madawwami. 8 Amma ga waɗanda suke sonkai waɗanda suke ƙin gaskiya suke kuma
bin mugunta, akwai fushi da haushi dominsu. 9 Akwai wahala da baƙin ciki ga duk
mutumin da yake aikata mugunta, da farko Yahudawa, sa'an nan Al'ummai, 10 amma
akwai ɗaukaka, girma da salama ga duk mutumin da yake aikata alheri, da farko
Yahudawa, sa'an nan Al'ummai. 11 Gama Allah ba ya nuna bambanci.
12 Duk waɗanda suka yi zunubi a rashi sanin doka, a rashin doka za su hallaka,
waɗanda kuma suka yi zunubi ƙarƙashin doka, a ƙarƙashin doka za a hukunta su.
13 Gama ba masu jin dokar ne suke da adalci a gaban Allah ba, amma waɗanda suke
yin biyayya da dokar, su za a ce da su masu adalci. 14 Tabbatacce, sa'ad da Al'ummai,
waɗanda ba su da dokar, suka aikata abubuwan da dokar take bukata, abubuwan
sun zama doka ke nan gare su, ko da yake ba su da dokar. 15 To, da yake sun nuna
cewa abubuwan da dokar take bukata suna a rubuce a zukatansu, lamirinsu yana

* **2:6** Zab 62.12; K Mag 24.12

kuma ba da shaida, tunaninsu kuwa yanzu yana zarginsu ko kuma yana kāre su.
16 Wannan zai faru a ranar da Allah ta wurin Yesu Kiristi zai shari'anta ɓoyayyun
abubuwan da mutane suka yi, yadda bisharata ta furta.

### *Yahudawa da doka*

17 To, kai, da kake kiran kanka mutumin Yahuda; in kana dogara ga doka kana
kuma taƙama da dangantakarka da Allah; 18 in ka san nufinsa ka kuma amince da
abin da yake mafifici domin an koyar da kai bisa ga doka; 19 in ka tabbata cewa kai
jagora ne ga makafi, haske ga waɗanda suke cikin duhu, 20 mai koyar da masu wauta,
malamin jarirai, domin a cikin dokar ce akwai sani da gaskiya 21 to, kai mai koya wa
waɗansu, ba kanka kake koya wa ba? Kai da kake wa'azi kada a yi sata, kana sata?
22 Kai da kake cewa wa mutane kada su yi zina, kana yin zina? Kai da kake ƙyamar
gumaka, kana wa haikali fashi? 23 Kai da kake taƙama da doka, kana nuna rashin
bangirma ga Allah ta wurin karya dokar? 24 Kamar yadda yake a rubuce, "Ana saɓon
sunan Allah a cikin Al'ummai saboda ku."†

25 Kaciya tana da amfani in kana kiyaye dokar, amma in kana karya dokar, ka zama
kamar ba a yi maka kaciya ba. 26 In marasa kaciya suna kiyaye dokar, ashe, ba za a
ɗauke su kamar an yi musu kaciya ba? 27 Wanda ba shi da kaciya ta jiki duk da haka
yana biyayya da dokar zai iya hukunta ka, kai da kake karya dokar, ko da yake kana
da rubutaccen tsarin dokar an kuma yi maka kaciya.

28 Mutum ba mutumin Yahuda ba ne in shi mutumin Yahuda ne kawai a jiki, haka
kuma kaciya ba a waje ko a jiki kawai ba. 29 A'a, mutum mutumin Yahuda ne in shi
mutumin Yahuda ne a zuci; kuma kaciya ita ce kaciya ta zuci, ta wurin Ruhu, ba ta
wurin rubutaccen doka ba. Irin wannan mutum yana samun yabo daga Allah ne, ba
ɗan adam ba.

# 3

### *Amincin Allah*

1 To, mece ce ribar zama mutumin Yahuda, ko kuwa mene ne amfanin kaciya?
2 Akwai riba ƙwarai ta kowace hanya! Da farko dai, su ne aka danƙa wa kalmomin
nan na Allah.

3 Amma a ce waɗansu ba su da bangaskiya fa? Rashin bangaskiyarsu nan zai shafe
amincin Allah? 4 Ko kaɗan! Bari Allah yă zama mai gaskiya, kowane mutum kuma
yă zama maƙaryaci. Kamar yadda yake a rubuce cewa,

"Gama a tabbatar kana da gaskiya, sa'ad da ka yi magana,
ka kuma yi nasara sa'ad da ka yi shari'a."*

5 Amma in rashin adalcinmu ya bayyana adalcin Allah a fili, me za mu ce ke nan?
Za mu ce Allah ya yi rashin adalci ke nan da ya saukar da fushinsa a kanmu? (Ina
magana kamar yadda mutum zai yi ne.) 6 Sam, ko kusa! Da a ce haka ne, ta yaya
Allah zai shari'anta duniya? 7 Wani zai iya ce, "In a dalilin ƙaryata, gaskiyar Allah
ta ƙara bayyana, har aka ƙara ɗaukaka shi, to, ta yaya zan zama mai zunubi, in
ƙaryata tana kawo ɗaukaka ga Allah?" 8 In haka ne, "Ba sai mu yi ta yin mugunta
don yă zama hanyar samun nagarta ba"? Kamar yadda masu baƙar magana game
da mu suna cewa wai haka muke faɗa. Tabbatacce za a hukunta irin waɗannan da
hukuncin da ya dace da su.

### *Babu mai adalci*

9 To, me za mu ce ke nan? Mun fi su ke nan? Ina, ko kaɗan! Mun riga mun zartar
cewa da Yahudawa da Al'ummai duk suna a ƙarƙarshin zunubi. 10 Kamar yadda
yake a rubuce cewa,

† **2:24** Ish 52.5; Ezk 36.22 * **3:4** Zab 51.4

"Babu wani mai adalci, babu ko ɗaya;
[11] babu wani mai fahimta,
babu wani mai neman Allah.
[12] Duk sun kauce gaba ɗaya,
sun zama marasa amfani;
babu wani mai aikata nagarta,
babu ko ɗaya."†
[13] "Maƙogwaronsu kamar buɗaɗɗun kaburbura ne,
harsunansu suna yin ƙarya."‡
"Dafin mugun maciji yana a leɓunansu."§
[14] "Bakunansu sun cike da la'ana da ɗacin rai."*
[15] "Kafafunsu suna saurin kai su zuwa ga zub da jini;
[16] hallaka da baƙin ciki suna ko'ina a hanyoyinsu,
[17] ba su kuma san hanyar salama ba."†
[18] "Babu tsoron Allah a idanunsu."‡
[19] Yanzu mun san cewa dukan abin da doka ta ce, tana magana ne ga waɗanda suke
ƙarƙarshin doka, saboda a rufe kowane baki; dukan duniya kuma ta ba da lissafin
kanta a gaban Allah. [20] Saboda haka babu wanda Allah zai ce da shi mai adalci ta
wurin kiyaye doka kawai; a maimako, ta wurin doka ne muke sane da zunubi.

*Adalci ta wurin bangaskiya*

[21] Amma yanzu an bayyana wani adalci daga Allah, wannan adalcin bai danganta
ga doka ba, Doka da Annabawa suna ba da shaida game da wannan adalci. [22] Wannan
adalcin Allah yana zuwa ta wurin bangaskiya a cikin Yesu Kiristi ga dukan waɗanda
suka ba da gaskiya ne. Ba bambanci, [23] gama duka sun yi zunubi suka kuma kāsa ga
ɗaukakar Allah, [24] an kuma kuɓutar da su kyauta ta wurin alherinsa bisa ga aikin
fansar da ya zo ta wurin Yesu Kiristi. [25] Allah ya miƙa Yesu Kiristi a matsayin hadayar
kafara, ta wurin bangaskiya cikin jininsa. Ya yi haka domin yă nuna adalcinsa, domin
a cikin haƙurinsa bai hukunta zunuban da aka aikata a dā ba [26] ya yi haka domin
yă nuna adalcinsa a wannan lokaci, saboda yă zama mai adalci da mai kuɓutar da
waɗanda suke ba da gaskiya a cikin Yesu.
[27] To, me za mu yi taƙama a kai? Babu wani abin da zamu yi taƙama a kai. A
kan wace ƙa'ida ce za mu yi taƙama? Ta hanyar bin doka ne? A'a, sai dai ta wurin
bangaskiya. [28] Gama mun tsaya a kan cewa ta wurin bangaskiya ne ake kuɓutar da
mutum, ba ta wurin kiyaye doka ba. [29] Allah ɗin, Allahn Yahudawa ne kaɗai? Shi
ba Allahn Al'ummai ba ne? I, shi Allahn Al'ummai ne ma, [30] da yake Allah ɗaya ne
kaɗai, shi kuma zai kuɓutar da masu kaciya bisa ga bangaskiya da kuma marasa
kaciya ta wurin wannan bangaskiya ɗin. [31] To, za mu soke dokar saboda wannan
bangaskiyar ne? Ko kaɗan! A maimako, sai ma tabbatar da ita muke yi.

# 4

*Adalcin Ibrahim ta wurin bangaskiya*

[1] To, me za mu ce Ibrahim kakan kakanninmu ya gani game da wannan batu? [2] In
fa da gaske ne Ibrahim ya sami kuɓuta ta wurin ayyuka, yana da abin da zai yin
taƙama da shi ke nan, amma ba a gaban Allah ba. [3] Me Nassin ya ce? "Ibrahim ya
gaskata Allah, aka kuma lissafta wannan adalci ne a gare shi."*
[4] To, sa'ad da mutum ya yi aiki, ba a lissafta ladan aikinsa a matsayin kyauta, sai dai
a matsayin hakkinsa. [5] Amma fa, game da mutumin da ba ya aiki sai dai dogara ga

† **3:12** Zab 14.1-3; Zab 53.1-3; M Had 7.20 ‡ **3:13** Zab 5.9 § **3:13** Zab 140.3 * **3:14** Zab 10.7 † **3:17** Ish 59.7,8 ‡ **3:18** Zab 36.1 * **4:3** Fit 15.6; haka da ma a aya 22

Allah wanda yake kuɓutar da masu mugunta, akan lissafta bangaskiyarsa a matsayin
adalci ne. 6 Dawuda ya faɗi haka sa'ad da ya yi magana game da albarkar da aka yi
wa mutumin da Allah ya lissafta adalci a gare shi, ba don yǎ yi ayyuka ba.
7 "Masu albarka ne
wanɗanda aka gafarta laifofinsu,
wanɗanda aka kuma rufe zunubansu.
8 Mai albarka ne mutumin
da Ubangiji ba zai taɓa lissafta zunubansa ba."†
9 Shin, wannan albarkar a kan masu kaciya ne kawai, ko kuwa har da marasa
kaciya ma? Mun sha faɗi cewa an lissafta bangaskiyar Ibrahim adalci ne a gare shi.
10 A kan wane hali ne aka lissafta masa? Bayan da aka yi masa kaciya ne, ko kuwa
kafin kaciyar? Ba bayan an yi masa kaciya ba ne, amma kafin a yi masa kaciya! 11 Ya
kuma karɓi alamar kaciya, hatimin adalcin da yake da shi ta wurin bangaskiya tun
yana marar kaciya. Saboda haka fa, ya zama mahaifin dukan wanɗanda suka gaskata
domin su ma a lasafta su masu adalci ne, ba tare da an yi musu kaciya ba. 12 Ya kuma
zama mahaifin masu kaciya wanɗanda ba kaciya kaɗai suke da ita ba amma har ma
suna bin gurbin bangaskiyar da mahaifinmu Ibrahim yake da ita kafin aka yi masa
kaciya.
13 Ba ta wurin doka ce Ibrahim da zuriyarsa suka sami alkawarin cewa zai zama
magājin duniya ba, amma sai dai ta wurin adalcin da yake zuwa ta wurin bangaskiya.
14 Gama da a ce masu kiyaye doka ne magāda, ai, da bangaskiya ba ta da amfani,
alkawarin kuma ya zama banza, 15 domin doka tana jawo fushi ne. Kuma inda babu
doka babu keta umarni ke nan.
16 Saboda haka, alkawari yakan zo ta wurin bangaskiya ne, domin yǎ zama ta wurin
alheri, don a tabbatar wa dukan zuriyar Ibrahim ba kawai ga wanɗanda suke na doka
ba amma har ma ga wanɗanda suke na bangaskiyar Ibrahim. Shi ne kuwa mahaifinmu
duka. 17 Kamar yadda yake a rubuce cewa, "Na mai da kai uban al'ummai masu
yawa."‡ Shi ubanmu ne a gaban Allah, wanda a cikinsa ya gaskata, Allahn da yake
ba da rai ga matattu, yake kuma kiran abubuwan da ba su kasance ba su zama kamar
sun kasance.
18 Saɓanin dukan bege, Ibrahim cikin bege ya gaskata, haka kuwa ya zama uban
al'ummai masu yawa, kamar yadda aka riga aka faɗa masa cewa, "Haka zuriyarka
za tǎ zama."§ 19 Ba tare da ya bar bangaskiyarsa ta yi rauni ba, ya fuskanci gaskiyan
nan mai cewa jikinsa mai tsufa matacce ne, da yake yana da shekara wajen ɗari,
mahaifar Saratu kuma matacciya ce. 20 Duk da haka bai yi shakka ta wurin rashin
bangaskiya game da alkawarin Allah ba, sai ma ya ƙara ƙarfafa ga bangaskiyarsa, ya
kuma ɗaukaka Allah, 21 yana kuma da cikakken tabbaci cewa Allah yana da iko yǎ
cika abin da ya yi alkawari. 22 Shi ya sa, "aka lissafta adalci a gare shi." 23 Kalmomin
nan, "aka lissafta a gare shi" ba a rubuta su saboda shi kaɗai ba ne, 24 amma saboda
mu ma, mu da Allah zai lissafta adalci, mu da muka ba da gaskiya gare shi da ya tashe
Yesu Ubangijinmu daga matattu. 25 An miƙa shi ga mutuwa saboda zunubanmu, aka
kuma tashe shi zuwa rai saboda Allah zai same mu marasa laifi.

# 5

*Salama da farin ciki*

1 Saboda haka, da yake an same mu marasa laifi ta wurin bangaskiya, muna* da
salama tare da Allah ta wurin Ubangijinmu Yesu Kiristi, 2 ta wurinsa ne muka sami
shiga wannan alherin da muke tsaye yanzu, ta wurin bangaskiya. Muna kuma† farin
ciki a begen ɗaukakar Allah. 3 Ba haka kawai ba, amma muna‡ kuma da farin ciki

† **4:8** Zab 32.2 ‡ **4:17** Far 17.5 § **4:18** Far 15.5 * **5:1** Ko kuwa bari mu † **5:2** Ko kuwa bari mu ‡ **5:3** Ko kuwa bari mu

cikin shan wuyanmu, gama mun san cewa shan wuyan nan takan haifi jimiri; 4 jimiri
kuma yakan kawo hali mai kyau; hali mai kyau kuma yakan sa bege. 5 Bege kuwa
ba ya ba mu kunya, domin Allah ya zuba ƙaunarsa a zukatanmu ta wurin Ruhu Mai
Tsarkin da ya ba mu.
6 Kun ga, a daidai lokaci, yayinda muke marasa ƙarfi, Kiristi ya mutu saboda
waɗanda ba su san Allah ba. 7 Da ƙyar wani yǎ mutu saboda mai adalci, ko da yake
saboda mutumin kirki wani zai iya ƙarfin hali yǎ mutu. 8 Amma Allah ya nuna mana
ƙaunarsa a wannan. Tun muna masu zunubi tukuna, Kiristi ya mutu dominmu.
9 Da yake yanzu mun sami zama marasa laifi ta wurin jininsa, ashe kuwa za a cece
mu daga fushin Allah ta wurinsa! 10 Gama in kuwa, sa'ad da muke abokan gāban
Allah, aka sulhunta mu da shi ta wurin mutuwar Ɗansa, ashe, da yake an sulhunta
mu, za mu sami ceto ta wurin ransa! 11 Ba ma haka yake kawai ba, har muna farin
ciki da Allah ta wurin Ubangijinmu Yesu Kiristi, wanda ta wurinsa yanzu muka sami
sulhu.

### *Mutuwa ta wurin Adamu, rai ta wurin Kiristi*

12 Saboda haka, kamar yadda zunubi ya shigo duniya ta wurin mutum ɗaya,
mutuwa kuma ta wurin zunubi, ta haka kuwa mutuwa ta shafi dukan mutane, domin
dukan mutane sun yi zunubi.
13 Gama kafin a ba da doka, zunubi yana nan a duniya. Amma ba a lissafin zunubi
inda babu doka. 14 Duk da haka, mutuwa ta yi mulki tun Adamu har yǎ zuwa Musa,
ta yi mulki har ma a kan waɗanda ba su yi zunubi ta wurin taka umarni kamar
yadda Adamu ya yi ba. A wata hanya dai Adamu shi ne kwatancin wani mutumin
nan mai zuwa.
15 Amma kyautan nan dabam take da laifin nan. Gama in mutane da yawa sun
mutu saboda laifin mutum ɗayan nan, to, ai, alherin Allah da kuma kyautan nan
mai zuwa ta wurin alherin mutum ɗayan nan, Yesu Kiristi, ya shafi mutane da yawa!
16 Kyautar Allah kuwa ba kamar sakamakon da ya bi zunubin mutum gudan nan
ba ne, Hukuncin ya bi zunubin mutum gudan nan, ya kuma kawo hallaka, amma
kyautar ta bi laifofin masu yawa ta kuma sa Allah ya gan mu a matsayin marasa laifi.
17 Gama in, ta wurin laifin mutum ɗaya, mutuwa ta yi mulki ta wurin mutum ɗayan
nan, ashe, waɗanda suka sami kyautar alherin Allah a yalwace da kuma kyautar
adalci za su yi mulki a wannan rayuwa ta wurin mutum ɗayan nan, Yesu Kiristi.
18 Saboda haka, kamar yadda sakamakon laifin mutum guda ya jawo hallaka ga
dukan mutane, haka ma sakamakon aikin adalci guda ya sa Allah ya same mu marasa
laifi, wannan kuwa kawo rai ga dukan mutane. 19 Gama kamar yadda ta wurin rashin
biyayyar mutum guda, mutane masu yawa suka zama masu zunubi, haka kuma ta
wurin biyayyar mutum guda, mutane da yawa za su zama masu adalci.
20 An ba da dokar don mu ga yadda laifi yake da girma. Amma da zunubi ya ƙaru,
sai alheri ya ƙaru sosai, 21 domin, kamar yadda zunubi ya yi mulki cikin mutuwa,
haka ma alheri yǎ yi mulki ta wurin adalci yǎ kuwa kawo rai madawwami ta wurin
Yesu Kiristi Ubangijinmu.

# 6

### *Matacce ga zunubi, rayayye a cikin Kiristi*

1 Me za mu ce ke nan? Za mu ci gaba da yin zunubi domin alheri yǎ haɓaka? 2 Sam,
ko kaɗan! Mun mutu ga zunubi; ta yaya za mu ci gaba da rayuwa a cikinsa kuma?
3 Ko ba ku sani ba cewa dukanmu da aka yi wa baftisma a cikin Kiristi Yesu an yi
mana baftismar ne zuwa cikin mutuwarsa? 4 Saboda haka, an binne mu da shi ke
nan, ta wurin baftisma cikin mutuwarsa, domin kamar yadda aka tā da Kiristi daga
matattu ta wurin ɗaukakar Uba, haka mu ma mu yi zaman sabuwar rayuwa.

5 In kuwa mun zama ɗaya tare da shi haka a cikin mutuwarsa, tabbatacce mu ma
za mu zama ɗaya tare da shi cikin tashinsa daga matattu. 6 Gama mun san cewa
an gicciye halayenmu na dā tare da shi domin a kawar da jikin nan mai zunubi don
kada mu ƙara zama bayi ga zunubi 7 domin duk wanda ya mutu an ʼyantar da shi
daga zunubi ke nan.
8 To, in mun mutu tare da Kiristi, mun gaskata cewa za mu rayu tare da shi kuma.
9 Gama mun san cewa da yake an tā da Kiristi daga matattu, ba zai sāke mutuwa ba;
mutuwa ba ta da sauran iko a kansa. 10 Mutuwar da ya yi, ya mutu ne sau ɗaya tak,
saboda yă shafe zunubi, amma rayuwar da yake yi, yana yi ne cikin tarayya da Allah.
11 Haka ku ma, ku ɗauke kanku matattu ne ga ikon zunubi amma rayayyu cikin
tarayya da Allah cikin Kiristi Yesu. 12 Saboda haka kada ku bar zunubi yă mallaki
jikin nan naku mai mutuwa yă sa ku zama masu biyayya ga mugayen shaʼawace-
shaʼawacensa. 13 Kada ku miƙa gaɓoɓin jikinku ga zunubi a matsayin kayan aikin
mugunta, sai dai ku miƙa kanku ga Allah, a matsayin waɗanda aka fitar da su daga
mutuwa zuwa rai; ku kuma miƙa gaɓoɓin jikinku gare shi a matsayin kayan aikin
adalci. 14 Gama zunubi ba zai zama maigidanku ba, domin ba kwa ƙarƙashin doka,
sai dai ƙarƙashin alheri.

*Bayi ga adalci*

15 Me za mu ce ke nan? Za mu ci gaba yin zunubi domin ba ma ƙarƙashin doka
sai dai ƙarƙashin alheri? Sam, ko kaɗan! 16 Ba ku sani ba cewa saʼad da kuka miƙa
kanku ga wani don ku yi masa biyayya a matsayin bayi, ko ku bayi ne ga zunubi,
wanda yake kai ga mutuwa, ko kuwa ga biyayya, wadda take kai ga adalci, ashe, ba
kun zama bayi ga wannan da kuke yi wa biyayya ba ke nan? 17 Amma godiya ga Allah
don ko da yake a dā ku bayi ne ga ikon zunubi, da dukan zuciyarku kun yi biyayya
ga irin koyarwar da aka danƙa muku. 18 An ʼyanta ku daga zunubi, kun kuma zama
bayi ga aikin adalci.
19 Ina magana ne kamar mutane saboda kun raunana a jikinku. Kamar yadda
kuka saba miƙa gaɓoɓin jikinku a bautar abubuwan ƙazanta da mugun aiki a kan
mugun aiki, saboda haka yanzu sai ku miƙa su bayi ga aikin adalci mai kai ga zaman
tsarki. 20 Saʼad da kuke bayin zunubi, ba ruwanku da aikin adalci. 21 Wace riba ce
kuka samu a lokacin, daga abubuwan nan da yanzu suka zama muku abin kunya?
Karshen irin abubuwan nan dai, mutuwa ne! 22 Amma a yanzu da aka ʼyantar da ku
daga zunubi kuka kuma zama bayi ga Allah, ribar da kuka samu tana kai ga zaman
tsarki, ƙarshenta kuwa rai madawwami ne. 23 Gama sakamakon zunubi mutuwa ne,
amma kyautar Allah rai madawwami ne a cikin Kiristi Yesu Ubangijinmu.

# 7

*Misali daga aure*

1 Ba ku sani ba, ʼyanʼuwa, ina magana ne fa da mutanen da suka san doka, cewa
dokar tana da iko a kan mutum muddin yana a raye ne kawai. 2 Misali, bisa ga doka
mace mai aure tana daure ga mijinta muddin mijin yana da rai, amma in mijinta ya
mutu, an sake ta ke nan daga dokar aure. 3 Saboda haka fa, in ta auri wani yayinda
mijinta yana raye, za a ce da ita mazinaciya. Amma in mijinta ya mutu, an sake ta
ke nan daga wannan doka, ita kuwa ba mazinaciya ba ce, ko da yake ta auri wani.
4 Saboda haka ʼyanʼuwana, ku ma kun mutu ga dokar ta wurin jikin Kiristi, domin
ku zama na wani, gare shi wanda aka tashe shi daga matattu, don mu ba da amfani
ga Allah. 5 Gama saʼad da halin mutuntaka yake mulkinmu, shaʼawace-shaʼawacen
zunubi waɗanda dokar ta zuga sun yi ta aiki a jikunanmu, don mu ba da amfani
wa mutuwa. 6 Amma yanzu, ta wurin mutuwa ga abin da dā ya daure mu, an sake

mu daga dokar saboda mu yi hidima a sabuwar hanyar Ruhu, ba a tsohuwar hanyar rubutaccen ƙa'ida ba.

*Yin fama da zunubi*

7 Me za mu ce ke nan? Dokar zunubi ce? Sam, ko kaɗan! Tabbatacce ai, da ban
san mene ne zunubi ba in ba ta wurin doka ba. Gama da ban san mene ne ƙyashi
yake ba tabbatacce in ba don doka ta ce, "Kada ka yi ƙyashi ba."* 8 Amma zunubi, da
ya sami dama ta wurin umarnin nan, ya haifar a cikina kowane halin ƙyashi iri-iri.
Gama in babu doka, zunubi matacce ne. 9 Dā kam ina da rai sa'ad da ban san doka
ba; amma da umarni ya zo, sai zunubi ya zaburo da rai na kuma mutu. 10 Na gane
cewa wannan umarnin da aka nufa ya kawo rai, a gaskiya ya jawo mutuwa ce.
11 Gama zunubi, da ya sami dama ta wurin umarni, sai ya ruɗe ni, kuma ta wurin
umarnin kuwa ya kashe ni. 12 Saboda haka fa, dokar tana da tsarki, umarnin kuma
yana da tsarki, su duka suna da adalci da kuma kyau.
13 Abin nan da yana mai kyau, zai kawo mini mutuwa? Ko kaɗan! Amma domin
zunubi ya bayyana kansa a matsayin zunubi, sai ya haifar da mutuwa a cikina ta
wurin abin da yake mai kyau, domin ta wurin umarnin nan zunubi ya fito da matuƙar
muninsa.
14 Mun san cewa doka aba ce ta ruhu; amma ni ba na ruhu ba ne, an sayar da ni
a matsayin bawa ga zunubi. 15 Ban gane abin da nake yi ba. Don abin da nakan so
yi, ba shi nakan yi ba, sai dai abin da nake ƙi, shi nake yi. 16 In kuma na yi abin da
ba na son yi, na yarda da cewa dokar aba ce mai kyau. 17 Kamar dai yadda yake, ba
ni kaina nake yinsa ba, sai dai zunubin da yake zaune a cikina ne. 18 Gama na san
cewa babu wani abin kirkin da yake zaune a cikina, wato, a mutuntakata.† Gama
sha'awar yin abu mai kyau kam ina da ita, sai dai ikon yin ne fa babu. 19 Gama abin
da nake yi ba shi ne abu mai kyau da nake so in yi ba; a'a, mugun da ba na so in
yi, shi ne nake ci gaba da yi. 20 To, in na yi abin da ba na so in yi, ba ni ba ne nake
yinsa, sai dai zunubin nan da yake zaune a cikina.
21 Saboda haka na gane wannan ƙa'ida ce take aiki a cikina. Sa'ad da nake so in yi
abu mai kyau, sai in ga cewa mugun nan ne nake yi. 22 Gama a ciki-cikina ina farin
cikin da dokar Allah; 23 amma ina ganin wata doka tana aiki a gaɓoɓin jikina, tana
yaƙi da dokar hankalina, tana kuma sa in zama ɗaurarren dokar zunubin da take
aiki a gaɓoɓin jikina. 24 Kaitona! Wane ne zai cece ni daga wannan jiki mai mutuwa?
25 Godiya ga Allah ta wurin Yesu Kiristi Ubangijinmu!

Saboda haka fa, ni kaina a cikin hankalina, ni bawa ne ga dokar Allah, amma a mutuntaka, ni bawa ne ga dokar zunubi.

# 8

*Rai ta wurin Ruhu*

1 Saboda haka, yanzu babu hukunci don waɗanda suke cikin Kiristi Yesu, 2 gama
ta wurin Kiristi Yesu dokar Ruhu mai ba da rai ta 'yantar da ni daga Dokar Musa.
3 Gama abin da dokar ba tă iya yi saboda kāsawar mutuntaka ba, Allah ya yi shi
sa'ad da ya aiko da Ɗansa a kamannin mutum mai zunubi, don yă zama hadaya ta
zunubi. Ta haka, ya hukunta zunubi a cikin mutum mai zunubi. 4 Ya yi haka domin
yă cika bukatun adalcin doka a cikinmu, mu da ba ma rayuwa bisa ga mutuntaka,
sai dai bisa ga Ruhu.
5 Waɗanda suke rayuwa bisa ga mutuntaka sun kafa hankulansu a kan sha'awace-
shawa'acen jiki; amma waɗanda suke rayuwa bisa ga Ruhu sun kafa hankulansu
a kan abubuwan da Ruhu yake so. 6 Kwallafa rai ga al'amuran halin mutuntaka

* **7:7** Fit 20.17; M Sh 5.21 † **7:18** Ko kuwa jikina

ƙarshensa mutuwa ne, ƙwallafa rai ga al'amuran Ruhu kuwa rai ne da salama;
[7] hankalin mai zunubi na gāba da Allah. Ba ya biyayya da dokar Allah, ba kuwa
zai iya yin haka ba. [8] Waɗanda mutuntaka yake mulkinsu ba za su iya su gamshi
Allah ba.
[9] Ku kam, ana mulkinku ba ta wurin mutuntaka ba, sai dai ta wurin Ruhu, in Ruhun
Allah yana zaune a cikinku. In kuma wani ba shi da Ruhun Kiristi, shi ba na Kiristi
ba ne. [10] Amma in Kiristi yana a cikinku, jikinku matacce ne saboda zunubi, duk da
haka ruhunku yana a raye saboda adalci. [11] In kuwa Ruhu wannan da ya tā da Yesu
daga matattu yana zama a cikinku, shi wanda ya tā da Kiristi daga matattu zai ba da
rai ga jikunanku masu mutuwa ta wurin Ruhunsa, wanda yake zama a cikinku.
[12] Saboda haka 'yan'uwa, muna da hakki, amma ba na wanda za mu yi rayuwar
mutuntaka da yake so ba. [13] Gama in kuna rayuwa bisa ga mutuntaka, za ku mutu;
amma in ta wurin Ruhu kuka kashe ayyukan jikin nan, za ku rayu.
[14] Domin waɗanda Ruhun Allah yake bi da su ne 'ya'yan Allah. [15] Gama ba ku
karɓi ruhun da ya mai da ku bayi da za ku sāke jin tsoro ba ne, sai dai kun karɓi
Ruhun zaman ɗa. Ta wurinsa kuwa muke kira, "*Abba,*[*] Uba." [16] Ruhu kansa yana ba
da shaida tare da ruhunmu cewa mu 'ya'yan Allah ne. [17] In kuwa mu 'ya'ya ne, to,
mu magāda ne, magādan Allah da kuma abokan gādo tare da Kiristi, in kuwa muna
tarayya a cikin shan wuyarsa to, za mu yi tarayya a cikin ɗaukakarsa.

### *Daukaka ta nan gaba*

[18] A ganina, wuyar da muke sha a wannan lokaci ba su isa a kwatanta da ɗaukakar
da za a bayyana a cikinmu ba. [19] Halitta tana jira da marmari ta ƙosa ta ga
bayyanuwar 'ya'yan Allah. [20] Gama an sa halitta a cikin wulaƙanci, ba da son ta
ba, sai dai ta wurin nufin wannan da ya mai da ita haka, da bege [21] cewa za a 'yantar
da halitta kanta daga bautarta ga ruɓewa a kuma kawo ta cikin 'yancin ɗaukakar
'ya'yan Allah.
[22] Mun san cewa dukan halitta tana nishi sai ka ce mace mai naƙuda har yă zuwa
wannan lokaci. [23] Ba haka kaɗai ba ma, mu kanmu da muke da nunan fari na Ruhu,
muna nishi a ciki-cikinmu yayinda muke jira da marmari a maishe mu 'ya'yan riƙo
na Allah, fansar jikunanmu. [24] Gama a wannan begen ne muka sami ceto. Amma
begen da ake gani ba bege ba ne sam. Wa yake begen abin da ya riga ya samu?
[25] Amma in muna begen abin da ba mu riga mun samu tukuna ba, mukan jira da
haƙuri.
[26] Haka nan ma, Ruhu yana taimakonmu cikin rashin ƙarfinmu. Ba mu san abin
da ya kamata mu roƙa cikin addu'a ba, amma Ruhu kansa yana roƙo a madadinmu
da nishe-nishen da kalmomi ba sa iya bayyanawa. [27] Shi kuma wanda yake binciken
zukatanmu ya san halin Ruhu, domin Ruhu yana roƙo a madadin tsarkaka bisa ga
nufin Allah.

### *Fiye da masu nasara*

[28] Mun kuma san cewa a cikin dukan abubuwa Allah yana aikata alheri ga waɗanda
suke ƙaunarsa,[†] yana[‡] waɗanda aka kira bisa ga nufinsa. [29] Gama waɗanda Allah
ya rigyasani ya kuma ƙaddara su dace da kamannin Ɗansa, don yă zama ɗan fari
cikin 'yan'uwa masu yawa. [30] Waɗanda kuwa ya ƙaddara, su ne ya kira; waɗanda
ya kira kuwa, su ne ya kuɓutar; waɗanda ya kuɓutar kuwa, su ne ya ɗaukaka.
[31] Me za mu ce ke nan game da wannan abu? In Allah yana goyon bayanmu, wa
kuwa zai iya gāba da mu? [32] Shi da bai hana Ɗansa ba, sai ma ya ba da shi saboda

---

[*] **8:15** Arameyik na Uba [†] **8:28** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da, A cikin dukan al'amura Allah [‡] **8:28** Ko kuwa aikata alheri ga waɗanda suke ƙaunarsa; waɗansu rubuce-rubucen hannu kuma suna da, dukan al'amura suna aikata tare zuwa ga alheri ga masu ƙaunar Allah

mu duka, ashe, ba zai kuma ba mu, tare da shi, dukan abubuwa cikin alherinsa ba?
33 Wa zai kawo wani zargi a kan waɗanda Allah ya zaɓa? Allah ne mai kuɓutarwa.
34 Wa zai yi hukunci? Yesu Kiristi ne, wanda ya mutu, fiye da haka ma, shi da aka tā
da zuwa rai, yana zaune a hannun dama na Allah yana kuma yin roƙo a madadinmu.
35 Wane ne zai raba mu da ƙaunar Kiristi? Masifa ce ko wahala ko tsanani ko yunwa
ko tsiraici ko hatsari ko takobi? 36 Kamar yadda yake a rubuce cewa,

“Saboda kai ne muke fuskantar mutuwa dukan yini;
an ɗauke mu kamar tumakin da za a yanka.”§

37 A'a, cikin dukan waɗannan abubuwa mun ma fi masu nasara ta wurin shi wanda
ya ƙaunace mu. 38 Gama na tabbata cewa ko mutuwa ko rai, ko mala'iku ko aljanu,
ko abubuwa na yanzu ko abubuwa masu zuwa nan gaba, ko ikoki, 39 ko tsayi ko zurfi,
ko wani abu dabam cikin dukan halitta da zai iya raba mu da ƙaunar Allah wadda
take cikin Kiristi Yesu Ubangijinmu.

# 9

### *Zaɓen Allah mai iko duka*

1 Ina faɗin gaskiya a cikin Kiristi ba ƙarya nake yi ba, lamirina ya tabbatar da
wannan a cikin Ruhu Mai Tsarki. 2 Ina da baƙin ciki mai yawa da kuma rashin
kwanciyar rai marar ƙarewa a zuciyata. 3 Gama da so na ne, sai a la'anta ni a kuma
raba ni da Kiristi saboda 'yan'uwana, waɗannan na kabilata, 4 mutanen Isra'ila. Su
ne Allah ya mai da su 'ya'yansa, ya bayyana musu ɗaukakarsa, ya ba su alkawarinsa
da Dokarsa, ya nuna musu hanyar sujada ta gaske, ya kuma ba su sauran alkawura.
5 Kakannin-kakannin nan kuma nasu ne, Kiristi kuma, ta wurin zamansa mutum, na
kabilarsu ne. Yabo ya tabbata ga Allah har abada, shi da yake bisa kome! Amin.

### *Zaɓin Allah mai iko duka*

6 Ba cewa maganar Allah ta kāsa ba ne. Gama ba duk waɗanda suke zuriyar
Isra'ila ne suke Isra'ila na gaske ba. 7 Ba kuwa don su zuriyarsa ne dukansu suka
zama 'ya'yan Ibrahim ba. A maimako, “Ta wurin Ishaku ne za a lissafta zuriyarka.”
8 Ana iya cewa zaman zuriyar Ibrahim, ba shi ne zama 'ya'yan Allah ba, a'a, zuriya
ta alkawarin nan su ne ake lasaftawa zuriyar Ibrahim. 9 Ga yadda aka yi alkawarin
nan, “A ƙayyadadden lokaci zan dawo, Saratu kuma za tă haifi ɗa.”*
10 Ba ma haka kaɗai ba, 'ya'yan Rifkatu suna da mahaifi guda ne, wato, mahaifinmu
Ishaku. 11 Duk da haka, tun ba a haifi tagwayen nan ba, balle su yi wani abu mai
kyau ko marar kyau don nufin Allah bisa ga zaɓensa ya tabbata, ba ga aikin lada ba,
sai dai ga kiransa, 12 ba ta wurin ayyuka ba sai dai ta wurin shi wanda ya kira, aka
faɗa mata cewa, “Babban zai bauta wa ƙaramin.”† 13 Kamar yadda yake a rubuce
cewa, “Yaƙub ne na so, amma Isuwa ne na ƙi.”‡
14 Me za mu ce ke nan? Allah marar adalci ne? Sam, ko kaɗan! 15 Gama ya ce wa
Musa,

“Zan nuna jinƙai ga wanda zan nuna jinƙai,
zan kuma ji tausayin wanda zan ji tausayi.”§

16 Saboda haka, bai danganta ga sha'awar mutum ko ƙoƙarinsa ba, sai dai ga jinƙan
Allah. 17 Gama Nassi ya ce wa Fir'auna, “Na ɗaga ka saboda wannan manufa, saboda
in nuna ikona a cikinka domin kuma a shaida sunana a duniya duka.”* 18 Saboda
haka Allah yana nuna jinƙai ga wanda yake so, yana kuma taurara zuciyar wanda
yake so.

---

§ **8:36** Zab 44.22 * **9:9** Far 18.10,14 † **9:12** Far 25.23 ‡ **9:13** Mal 1.2,3 § **9:15** Fit 33.19 * **9:17** Fit 9.16

19 Waninku zai iya ce mini, “To, don me har yanzu Allah yake ganin laifinmu?
Gama wa zai iya tsayayya da nufinsa?” 20 Amma wane ne kai, ya mutum, da za ka
mayar wa Allah magana? “Ashe, abin da aka gina zai iya ce wa wanda ya gina shi,
‘Don me ka gina ni haka?’ ”† 21 Ashe, mai ginin tukwane ba shi da iko yin amfani
da yumɓu guda yǎ gina tukunya domin ayyuka masu daraja da kuma waɗansu don
ayyuka marasa daraja?

22 Haka ma aikin Allah yake. Ya so yǎ nuna fushinsa yǎ kuma sanar da ikonsa, ya yi
haka cikin haƙuri ƙwarai ga waɗanda suka cancanci fushinsa, waɗanda aka shirya
domin hallaka? 23 Haka kuma ya so yǎ sanar da wadatar ɗaukakarsa ga waɗanda
suka cancanci jinƙansa, waɗanda ya shirya tun kafin lokaci don ɗaukaka 24 har da
mu ma, mu da ya kira, ba daga cikin Yahudawa kaɗai ba amma har ma daga cikin
Al’ummai? 25 Kamar yadda ya faɗa a Hosiya.

“Zan kira su ‘mutanena,’ su da ba mutanena ba;
zan kuma kira ta ‘ƙaunatacciyata,’ ita da ba ƙaunatacciyata ba,”‡
26 kuma,
“Zai zama cewa a daidai inda aka ce musu,
‘Ku ba mutanena ba,’
za a ce da su, ‘‘ya’yan Allah mai rai.’ ”§
27 Ishaya ya ɗaga murya game da Isra’ila ya ce,
“Ko da yake yawan Isra’ilawa yana kama da yashi a bakin teku,
ragowa ce kaɗai za su sami ceto.
28 Gama Ubangiji zai zartar da
hukuncinsa a bisan duniya da sauri kuma ba da ɓata lokaci ba.”*
29 Yana nan kamar yadda Ishaya ya riga ya faɗa.
“Da ba don Ubangiji Maɗaukaki
ya bar mana zuriya ba,
da mun zama kamar Sodom,
da mun kuma zama kamar Gomorra.”†

*Rashin bangaskiyar Isra’ila*

30 Me za mu ce ke nan? Ai, Al’ummai da ba su nemi adalci ba, sun same shi,
adalcin da yake ta wurin bangaskiya; 31 amma Isra’ila da suka yi ƙwazo wajen bin
Dokar adalci, ba su same shi ba. 32 Don me? Domin sun yi ƙwazo wajen binta ba
ta wurin bangaskiya ba sai dai ta wurin ayyuka. Sun yi tuntuɓe a kan “dutsen sa
tuntuɓe.” 33 Kamar yadda yake a rubuce,
“Ga shi, na sa dutse a Sihiyona da yake sa mutane yin tuntuɓe
da kuma dutsen da yake sa su fāɗi
wanda kuwa ya dogara gare shi ba zai taɓa shan kunya ba.”‡

# 10

1 ’Yan’uwa, abin da zuciyata take so da kuma addu’ata ga Allah saboda Isra’ilawa
shi ne su sami ceto. 2 Gama na shaida su a kan suna da kishi bin Allah, sai dai
kishinsu ba a bisa sani ba. 3 Da yake ba su san adalcin da yake fitowa daga Allah ba
suka kuma nemi su kafa nasu, sai suka ƙi miƙa kai ga adalcin Allah. 4 Kiristi shi ne
ƙarshen doka domin a sami adalci wa kowane mai bangaskiya.

5 Musa ya bayyana adalcin da yake ga Doka cewa, “Mutumin da ya aikata
waɗannan abubuwa zai rayu ta wurinsu.”* 6 Amma adalcin da yake ga bangaskiya
yana cewa, “Kada ka faɗa a zuciyarka, ‘Wa zai hau sama?’ ”† (wato, don yǎ sauko
da Kiristi), 7 “ko kuwa ‘Wa zai gangara can zurfin ƙasa?’ ” (wato, don yǎ hauro da

† **9:20** Ish 29.16; Ish 45.9 ‡ **9:25** Hos 2.23 § **9:26** Hos 1.10 * **9:28** Ish 10.22,23 † **9:29** Ish 1.9 ‡ **9:33** Ish 8.14; Ish 28.16 * **10:5** Fir 18.5 † **10:6** M Sh 30.13

Kiristi daga matattu). 8 Amma mene ne aka ce? “Maganar tana kusa da kai; tana cikin
bakinka da kuma cikin zuciyarka,”‡ wato, maganar bangaskiyan nan da muke shela.
9 Cewa in ka furta da bakinka, “Yesu Ubangiji ne,” ka kuma gaskata a zuciyarka
cewa Allah ya tā da shi daga matattu, za ka sami ceto. 10 Gama da zuciyarka ce
kakan gaskata a kuma kuɓutar da kai, da bakinka ne kuma kake furta a kuma cece
ka. 11 Kamar yadda Nassi ya ce, “Duk wanda ya gaskata da shi ba zai taɓa shan
kunya ba.”§ 12 Gama ba bambanci tsakanin mutumin Yahuda da mutumin Al’ummai,
Ubangijin nan ɗaya shi ne Ubangijin kowa yana kuma ba da albarka a yalwace ga
duk masu kira gare shi, 13 gama, “Duk wanda ya kira bisa sunan Ubangiji zai sami
ceto.”*
14 To, ta yaya za su kira ga wanda ba su gaskata ba? Ta yaya kuma za su gaskata
wanda ba su taɓa ji ba? Ta yaya kuma za su ji ba tare da wani ya yi musu wa’azi
ba? 15 Kuma ta yaya za su yi wa’azi in ba an aike su ba? Kamar yadda yake a rubuce
cewa, “Isowar masu kawo labari mai daɗi abu mai kyau ne ƙwarai!”†
16 Amma ba dukan Isra’ilawa ne suka karɓi labari mai daɗin nan ba. Gama Ishaya
ya ce, “Ubangiji, wa ya gaskata saƙonmu?”‡ 17 Saboda haka, bangaskiya takan zo
ne ta wurin jin saƙo, akan ji saƙon kuma ta wurin maganar Kiristi. 18 Amma ina
tambaya, “Ba su ji ba ne? Tabbatacce sun ji.

“Muryarsu ta tafi ko’ina a cikin duniya,
kalmominsu kuma har iyakar duniya.”§

19 Har wa yau, ina da tambaya. Shin, Isra’ila ba su fahimta ba ne? Da farko, Musa ya
ce,

“Zan sa ku yi kishin waɗanda ba al’umma ba;
zan sa ku yi fushin al’ummar da ba ta da fahimta.”*

20 Ishaya kuma ya fito gabagadi ya ce,

“Waɗanda ba su neme ni ba, su suka same ni;
Na bayyana kaina ga waɗanda ba su ma taɓa neman sanina ba.”

21 Amma game da Isra’ila ya ce,

“Dukan yini na miƙa hannuwana
ga mutane marasa biyayya da masu taurinkai.”†

# 11

*Ragowar Isra’ila*

1 To, ina da tambaya. Allah ya ƙi mutanensa ne? Sam, ko kaɗan! Ni mutumin
Isra’ila ne kaina, zuriyar Ibrahim kuwa, daga kabilar Benyamin. 2 Allah bai ƙi
mutanensa da ya rigya sani ba. Ba ku san abin da Nassi ya faɗa game da Iliya
ba, yadda ya kawo kuka ga Allah a kan Isra’ila ya ce, 3 “Ya Ubangiji, sun karkashe
annabawanka suka kuma rurrushe bagadanka; ni kaɗai na ragu, suna kuma neman
raina”*? 4 Wace amsa ce Allah ya ba shi? “Na keɓe wa kaina dubu bakwai waɗanda
ba su yi wa Ba’al sujada ba.”† 5 Haka ma, a wannan zamani akwai ragowar da aka
zaɓa ta wurin alheri. 6 In kuwa na alheri ne, ba sauran cewa ya dogara ga ayyuka
ke nan. In ba haka ba, ashe, alheri ba alheri ba ne kuma.
7 To, sai me? Abin da Isra’ila suka nema da himma ba su samu ba, amma zaɓaɓɓun
suka samu. Sauran suka taurare, 8 kamar yadda yake a rubuce cewa,

“Allah ya ba su ruhun ruɗewa,
idanu don su kāsa gani,
da kuma kunnuwa don su kāsa ji,

‡ **10:8** M Sh 30.14 § **10:11** Ish 28.16 * **10:13** Yow 2.32 † **10:15** Ish 52.7 ‡ **10:16** Ish 53.1 § **10:18** Zab 19.4 * **10:19** M Sh 32.21 † **10:21** Ish 65.2 * **11:3** 1Sar 19.10,14 † **11:4** 1Sar 19.18

har yă zuwa yau."‡
9 Dawuda kuma ya ce,
"Bari teburin cin abincinsu yă zama musu tarko,
sanadin fāɗuwa da dutsen sa tuntuɓe da kuma ramuwa a kansu.
10 Bari idanunsu su duhunta don kada su iya gani,
bayansu kuma yă tanƙware har abada."§

*Rassan aure*

11 Har yanzu ina da tambaya. Sun yi tuntuɓe har ya kai ga fāɗuwar da ba za su iya
tashi ba ne? Sam, ko kaɗan! A maimako, saboda laifinsu ne ceto ya zo ga Al'ummai
don a sa mutanen Isra'ila su ji kishi. 12 Amma in laifinsu yana nufin albarka ga
duniya, hasararsu kuma albarka ga Al'ummai, ina misalin yalwar da albarkunsu za
su kawo!
13 Ina magana da ku ne fa Al'ummai. Tun da yake ni manzo ne ga Al'ummai, ina
taƙama da aikin nan nawa, 14 da fata zan rura kabilata a ta kowace hanya su ji kishi
har ma yă sa in ceci waɗansunsu. 15 Gama in ƙinsu da aka yi ya zama sulhu ga
duniya, me karɓarsu za tă zama in ba rai daga matattu ba? 16 In sashen da aka miƙa
a matsayin nunan fari tsattsarka ne, to, sauran ma tsattsarka ne; in saiwar tsattsarka
ce, to, sauran rassan ma tsattsarka ne.
17 In an sassare waɗansu rassa, kai kuwa da kake kai zaitun jeji, aka ɗauke ka aka
kuma yi muku aure, a yanzu kuwa kana shan ni'imar saiwar zaitun ɗin nan tare
da sauran rassan, 18 kada ka yi taƙama cewa ka fi waɗancan rassan da aka sassare.
In kuwa ka yi haka, to, ka yi la'akari da wannan. Ba kai ne kake taimakon saiwar
ba, saiwar ce take taimakonka. 19 To, kana iya cewa, "An sassare rassan ne don a
ɗaura aure da ni." 20 Haka yake. Amma an sassare su ne saboda rashin bangaskiya,
kai kuma kana tsaye ta wurin bangaskiya. Kada ka yi taƙama, sai dai ka ji tsoro.
21 Gama in har Allah bai bar rassan nan na asali ba, kai ma ba zai bar ka ba.
22 Ka lura fa da alheri da kuma tsananin Allah, tsanani ga waɗanda suka fāɗi,
amma alheri a gare ka, da fata za ka ci gaba cikin alherinsa. In ba haka ba, kai ma
za a sare ka. 23 In kuwa ba su nace cikin rashin bangaskiya ba, za a sāke ɗaura aure
da su, domin Allah yana iya sāke haɗa su. 24 Kai ma da aka saro daga zaitun ɗin da
asalinsa yake na jeji, aka ɗaura aure da kai a jikin zaitun ɗin na gida, saɓanin yadda
aka saba, balle waɗannan rassa na asali, da za a ɗaura aure da su a jikin zaitun ɗin
nan nasu na asali?

*Dukan Isra'ila za su tsira*

25 Ba na so ku kasance cikin rashin sani game da wannan asirin 'yan'uwa, domin
kada ku ɗaga kai. Isra'ila sun ɗanɗana sashe na taurarewa har sai da shigowar
Al'ummai masu yawa ya cika. 26 Ta haka kuwa za a ceci dukan Isra'ila, kamar yadda
yake a rubuce cewa,
"Mai ceto zai zo daga Sihiyona;
zai kawar da rashin bin Allah daga Yaƙub.
27 Wannan kuwa shi ne alkawarina da su
sa'ad da na ɗauke musu zunubansu."*
28 Game da zancen nan na bishara kuwa, su abokan gāba ne saboda ku; amma game
da zaɓen kuwa, su ƙaunatattunsa ne, albarkacin kakannin kakanninsu, 29 gama
kyautar Allah da kiransa ba a sokewa. 30 Kamar yadda a dā can ku da kuke marasa
biyayya ga Allah kuka sami jinƙai yanzu ta dalilin rashin biyayyarsu, 31 haka su ma
suka zama marasa biyayya a yanzu domin su ma su sami jinƙai ta dalilin jinƙan da

‡ **11:8** M Sh 29.4; Ish 29.10 § **11:10** Zab 69.22,23 * **11:27** Ish 59.20,21; Ish 27.9; Irm 31.33,34

Allah ya yi muku. [32] Gama Allah ya daure dukan mutane ga rashin biyayya don yă
nuna jinƙai ga kowa.

### *Ɗaukakawa*

[33] Kai, zurfin yalwar hikima da kuma sanin Allah yana nan a yalwace!
Hukunce-hukuncensa kuma su fi gaban bincike,
hanyoyinsa kuwa sun wuce gaban ganewa!
[34] "Wa ya taɓa sanin zuciyar Ubangiji?
Ko kuwa yă ba shi shawara?"†
[35] "Wa ya taɓa ba wa Allah wani abu,
da Allah zai sāka masa?"‡
[36] Gama daga gare shi, ta wurinsa, da kuma saboda shi ne dukan abubuwa suka
kasance.
Ɗaukaka ta tabbata a gare shi har abada! Amin.

# 12

### *Hadayu masu rai*

[1] Saboda haka, ina roƙonku, 'yan'uwa, saboda yawan jinƙan Allah, ku miƙa
jikunanku hadaya wadda take mai rai, mai tsarki abin karɓa kuma ga Allah, wannan
ita ce hanyar hidimarku ta ruhaniya. [2] Kada ku ci gaba da yin abin da duniya take
yi, sai dai ku bar halinku ya sāke, ta wurin sabunta hankalinku ɗungum, don ku
tabbatar da abin da Allah yake so yake, abu mai kyau, mai daɗi da kuma cikakke.
[3] Gama ta wurin alherin nan da aka yi mini ne ina ce wa kowannenku. Kada yă
ɗauki kansa fiye da yadda ya kamata, a maimakon haka bari yă auna kansa cikin
natsuwa, gwargwadon baiwar bangaskiyar da Allah yi masa. [4] Kamar dai yadda
kowannenmu yake da jiki ɗaya da gaɓoɓi da yawa, gaɓoɓin nan kuwa ba aiki iri
ɗaya suke yi ba, [5] haka ma a cikin Kiristi mu da muke da yawa mun zama jiki
ɗaya, kuma kowace gaɓar ɗan'uwan sauran ne. [6] Muna da baye-baye dabam-dabam,
gwargwadon alherin da aka yi mana. In baiwar mutum ta yin annabci ce, sai yă yi
amfani da ita gwargwadon bangaskiyarsa. [7] In ta hidima ce; sai yă yi hidima. In kuma
ta koyarwa ce, sai yă koyar; [8] in ta ƙarfafawa ce, sai yă ƙarfafa; in kuma ta ba da
taimako ce don biyan bukatun waɗansu, sai yă yi haka hannu sake; in ta shugabanci
ce, sai yă yi shugabanci da himma; in ta nuna jinƙai ce, sai yă yi haka da fara'a.

### *Ƙauna*

[9] Dole ƙauna tă zama ta gaskiya. Ku ƙi duk abin da yake mugu; ku manne wa abin
da yake nagari. [10] Ku ba da kanku ga juna cikin ƙauna irin ta 'yan'uwa. Kowa yă yi
ƙoƙari wajen girmama wani fiye da kansa. [11] Kada ku zama marasa himma, sai dai
masu himma a ruhaniyarku, kuna bauta wa Ubangiji. [12] Ku yi farin ciki cikin bege,
haƙuri cikin shan wuya, aminci cikin addu'a. [13] Ku taimaki mutanen Allah masu
bukata. Ku zama masu karɓan baƙi.
[14] Ku sa wa masu tsananta muku albarka; ku sa albarka kada fa ku la'anta. [15] Ku
yi murna da masu murna, ku yi kuka da masu kuka. [16] Ku yi zaman lafiya da juna.
Kada ku nuna girman kai, sai ma ku riƙa cuɗanya da talakawa. Kada ku zama masu
ɗaga kai.
[17] Idan kowa ya yi muku mugunta, kada ku sāka masa da mugunta. Ku lura don
ku aikata abin da kowa zai iya gani cewa daidai ne. [18] Ku yi iya ƙoƙarinku, in zai
yiwu, ku yi zaman lafiya da kowa. [19] Kada ku yi ramuwa, abokaina, sai dai ku bar wa
Allah. Gama a rubuce yake cewa, "Ramuwa tawa ce; zan kuwa sāka,"* in ji Ubangiji.
[20] A maimakon haka,

† **11:34** Ish 40.13 ‡ **11:35** Ayu 41.11 * **12:19** M Sh 32.35

"In abokin gābanka yana jin yunwa, ka ciyar da shi;
in yana jin ƙishirwa, ka ba shi ruwan sha.
Ta yin haka, za ka tara garwashin wuta a kansa."†
21 Kada ku bar mugunta ta sha kanku, sai dai ku sha kan mugunta ta wurin aikata nagarta.

# 13

*Biyayya ga masu mulki*
1 Dole kowa yă yi biyayya ga masu mulki, gama babu wani iko sai ko in Allah ya
yarda. Duk hukumomin da muke su, naɗin Allah ne. 2 Saboda haka, duk wanda ya yi
tawaye ga hukuma yana yin tawaye da abin da Allah ya naɗa ne, waɗanda kuwa suke
aikata haka, za su jawo wa kansu hukunci. 3 Gama masu mulki ba abin tsoro ba ne
ga waɗanda suke yin abin da yake daidai, sai dai ga waɗanda suke aikata laifi. Kana
so ka rabu da jin tsoron wanda yake mulki? To, sai ka aikata abin da yake daidai,
zai kuwa yabe ka. 4 Gama shi bawan Allah ne don kyautata rayuwarka. Amma in ka
aikata mugunta, to, sai ka ji tsoro, don ba a banza ne shugaba yake ɗaukan takobinsa
ba. Shi fa bawan Allah ne, ta wurinsa ne fushin Allah yakan hukunta masu laifi.
5 Saboda haka, dole a yi biyayya ga hukumomi, ba don gudun horo kawai ba amma
don lamirinku.
6 Shi ne ma ya sa kuke biyan haraji, gama hukumomin nan bayin Allah ne, waɗanda
suke ba da dukan lokacinsu don aikin shugabanci. 7 Ku ba wa kowa hakkinsa. In kuna
da bashin haraji, sai ku biya; in kuɗin shiga ne, ku biya kuɗin shiga; in ladabi ne, ku yi ladabi; in kuma girmamawa ne, ku ba da girma.

*Ku yi ƙauna, gama ranar ta yi kusa*
8 Kada hakkin kowa yă zauna a kanku, sai dai na ƙaunar juna, don mai ƙaunar
maƙwabcinsa ya cika Doka ke nan. 9 Umarnan nan, "Kada ka yi zina." "Kada
ka yi kisankai." "Kada ka yi sata." "Kada kuma ka yi ƙyashi."* Da dai duk sauran umarnai an ƙunshe su ne a wannan kalma "Ka ƙaunaci maƙwabcinka kamar
kanka." 10 Kauna ba ta cutar da maƙwabci. Saboda haka ƙauna cika Doka ce.
11 Ku yi wannan domin kun san irin zamanin da kuke ciki. Lokaci ya yi da za ku
farka daga barcinku, don cetonmu ya yi kusa yanzu fiye da lokacin da muka fara ba
da gaskiya. 12 Dare fa ya kusan ƙarewa; gari kuma yana gab da wayewa. Saboda
haka bari mu kawar da ayyukan duhu mu kuma yafa kayan yaƙi na haske. 13 Bari
mu tafiyar da al'amuranmu yadda ya dace a yi da rana, ba a cikin shashanci da
buguwa ba, ba cikin fasikanci da rashin kunya ba, ba kuma cikin faɗa da kishi ba.
14 A maimakon haka, ku ɗauki halin Ubangiji Yesu Kiristi, kada kuma ku yi tunani game da yadda za ku gamsar da sha'awace-sha'awacen mutuntaka.

# 14

*Marasa ƙarfi da masu ƙarfi*
1 Ku karɓi wanda bangaskiyarsa ba tă yi ƙarfi ba, amma fa kada ku hukunta shi
a kan abubuwan da ake da shakka a kai ba. 2 Bangaskiyar mutum ta yarda masa
yă ci kome, amma wanda bangaskiyarsa ba tă yi ƙarfi ba, yakan ci kayan lambu ne
kawai. 3 Mutumin da yake cin kowane irin abinci, kada yă rena wanda ba ya cin,
wanda kuma ba ya cin kowane irin abinci, kada yă ga laifin mutumin da yake ci,
domin Allah ya riga ya karɓe shi. 4 Kai wane ne har da za ka ga laifin bawan wani?
Ko bawan yă yi aiki mai kyau, ko yă kāsa, ai, wannan ruwan maigidansa ne. Za a ma tsai da shi, domin Ubangiji yana da ikon tsai da shi.

† **12:20** K Mag 25.21,22 * **13:9** Fit 20.13-15,17; M Sh 5.17-19; M Sh 5.21

5 Wani yakan ɗauki wata rana da daraja fiye da sauran ranaku; wani kuma yana
ganin dukan ranakun ɗaya ne. Ya kamata kowa yă kasance da tabbaci a cikin
zuciyarsa. 6 Wannan mai ɗaukan rana ɗaya da muhimmanci fiye da sauran, yana
yin haka ne ga Ubangiji. Wannan mai cin nama, yana yin haka ne ga Ubangiji, gama
yakan yi godiya ga Allah; wannan da ba ya ci kuwa, yana yin haka ne ga Ubangiji
yana kuwa yin godiya ga Allah. 7 Gama ba waninmu da yake rayuwa wa kansa kaɗai,
kuma ba waninmu da kan mutu don kansa kaɗai. 8 In muna rayuwa, muna rayuwa
ne ga Ubangiji; in kuma muna mutuwa, muna mutuwa ne ga Ubangiji. Saboda haka,
ko muna a raye ko muna a mace, mu na Ubangiji ne. 9 Saboda wannan ne Kiristi ya
mutu, ya kuma sāke rayuwa domin yă zama Ubangiji na matattu da na masu rai.

10 Kai kuwa, don me kake ganin laifin ɗan'uwanka? Ko kuma don me kake rena
ɗan'uwanka? Gama duk za mu tsaya a gaban kujerar shari'ar Allah. 11 A rubuce
yake cewa,

" 'Muddin ina raye,' in ji Ubangiji,

'kowace gwiwa za tă durƙusa a gabana;

kowane harshe kuma zai furta wa Allah.' "*

12 Don haka kowannenmu zai ba da lissafin kansa ga Allah.

13 Saboda haka bari mu daina ba wa juna laifi. A maimakon, sai kowa yă yi niyya
ba zai sa dutsen tuntuɓe ko abin sa fāɗuwa a hanyar ɗan'uwansa ba. 14 A matsayina
na mai bin Ubangiji Yesu na tabbata ƙwarai cewa babu abincin da yake marar tsabta
don kansa. Amma in wani ya ɗauka wani abu marar tsabta ne, to, a gare shi marar
tsabta ne. 15 In kana ɓata wa ɗan'uwanka zuciya saboda abincin da kake ci, ba halin
ƙauna kake nunawa ba ke nan. Kada abincin da kake ci yă zama hanyar lalatar
da ɗan'uwanka wanda Kiristi ya mutu dominsa. 16 Kada ka bar abin da ka ɗauka
a matsayi kyakkyawa yă zama abin zargi ga waɗansu. 17 Gama mulkin Allah ba
batun ci da sha ba ne, sai dai na adalci, salama, da kuma farin ciki cikin Ruhu Mai
Tsarki, 18 duk kuwa wanda yake bauta wa Kiristi a haka yana faranta wa Allah rai
ne, yardajje kuma ga mutane.

19 Saboda haka sai mu yi iya ƙoƙari mu aikata abin da zai kawo salama da kuma
ingantawa ga juna. 20 Kada ku lalatar da aikin Allah saboda abinci. Dukan abinci
mai tsabta ne, sai dai ba daidai ba ne mutum yă ci abin da zai sa wani yă yi tuntuɓe.
21 Ya fi kyau kada ka ci nama ko ka sha ruwan inabi ko kuma ka yi wani abin da zai
sa ɗan'uwanka yă fāɗi.

22 Bari duk ra'ayin da kake da shi game da wannan sha'ani yă kasance tsakaninka
da Allah. Mai albarka ne wanda zuciyarsa ba tă ba shi laifi game da abin da shi da
kansa ya ɗauka cewa daidai ne ba. 23 Amma wanda yake da shakka yakan jawo wa
kansa hukunci ne in ya ci, domin yana ci ne ba bisa ga bangaskiya ba; kuma duk
abin da bai zo daga bangaskiya ba zunubi ne.

# 15

1 Mu da muke da ƙarfi ya kamata mu yi haƙuri da kāsawar marasa ƙarfi ba kawai
mu gamshi kanmu ba. 2 Ya kamata kowannenmu yă faranta wa maƙwabcinsa rai
don kyautata zamansa domin kuma yă gina shi. 3 Gama ko Kiristi ma bai gamshi
kansa ba, amma kamar yadda yake a rubuce cewa, "Zage-zagen da waɗansu suka yi
maka, duk sun fāɗo a kaina."* 4 Gama duk abin da aka rubuta a dā an rubuta ne
domin yă koya mana, don ta wurin jimrewa da kuma ƙarfafawar Nassosi mu kasance
da bege.

* **14:11** Ish 45.23 * **15:3** Zab 69.9

5 Bari Allah mai ba da haƙuri da kuma ƙarfafawa yă ba ku ruhun haɗinkai da juna
yayinda kuke bin Kiristi Yesu, 6 don da zuciya ɗaya da kuma baki ɗaya kuke ɗaukaka
Allah da kuma Uban Ubangijinmu Yesu Kiristi.
7 Ta haka sai ku karɓi juna kamar yadda Kiristi ya karɓe ku, don a yabi Allah. 8 Ina
dai gaya muku cewa Kiristi ya zama bawan Yahudawa a madadin gaskiyar Allah, don
yă tabbatar da alkawaran da aka yi wa kakannin kakanninmu 9 domin Al'ummai su
ɗaukaka Allah saboda jinƙansa, kamar yadda yake a rubuce,

"Saboda haka zan yabe ka a cikin Al'ummai;
zan rera waƙoƙi ga sunanka."†

10 Ya kuma ce,
"Ku yi farin ciki, ya Al'ummai, tare da mutanensa."‡

11 Da kuma,
"Ku yabi Ubangiji, dukanku Al'ummai,
ku kuma rera masa yabo, dukanku mutanen duniya."§

12 Kuma Ishaya ya ce,
"Tushen Yesse zai tsiro,
wanda zai taso yă yi mulkin al'ummai;
al'ummai za su sa bege a gare shi."*

13 Bari Allah na bege yă cika ku da matuƙar farin ciki da salama yayinda kuke
dogara gare shi, domin ku yalwata cikin bege ta wurin ikon Ruhu Mai Tsarki.

### *Bulus mai hidima ga al'ummai*

14 Ni kaina na tabbata, 'yan'uwana, cewa ku kanku kuna cike da kirki, cikakku
cikin sani da kuma ƙwararru don yin wa juna gargaɗi. 15 Na rubuta muku gabagadi
a kan waɗansu batuttuwa, don in sāke tuna muku su, saboda alherin da Allah ya
ba ni 16 in zama mai hidimar Kiristi Yesu ga Al'ummai da aikin firist na yin shelar
bisharar Allah, don Al'ummai su zama hadaya mai karɓuwa ga Allah, tsattsarka ta
wurin Ruhu Mai Tsarki.
17 Saboda haka ina taƙama cikin Kiristi Yesu a cikin hidimata ga Allah. 18 Ba zan
yi karambani in faɗi kome ba sai dai abin da Kiristi ya aikata ta wurina a jagorantar
da Al'ummai su yi biyayya ga Allah ta wurin abin da na faɗa da kuma aikata 19 ta
wurin ikon alamu da ayyukan banmamaki, da kuma ikon Ruhun Allah. Ta haka
daga Urushalima har yă zuwa kewayen Illirikum, na yi wa'azin bisharar Kiristi.
20 Labudda, burina shi ne in yi wa'azin bishara inda ba a san Kiristi ba, don kada
yă zama ina gini ne a kan tushen da wani ya kafa. 21 Sai dai kamar yadda yake a
rubuce,

"Waɗanda ba a faɗa musu labarinsa ba za su gani,
waɗanda kuma ba su ji ba za su fahimta."†

22 Wannan ne ya sa sau da yawa aka hana ni zuwa wurinku.

### *Shirin Bulus yă ziyarci Roma*

23 Amma yanzu da babu sauran wurin da ya rage mini in yi aiki a waɗannan
yankuna, da yake kuma shekaru masu yawa ina da marmari in gan ku, 24 ina shirin
yin haka in na tafi Sifen. Ina fata in ziyarce ku yayinda nake wucewa don ku raka
ni can, bayan na ji daɗin zama tare da ku na ɗan lokaci. 25 Yanzu kam, ina hanyata
zuwa Urushalima don in kai gudummawa ga tsarkaka a can. 26 Gama Makidoniya da
Akayya sun ji daɗin yin gudummawa domin matalautan da suke cikin tsarkakan da
suke a Urushalima. 27 Sun kuwa ji daɗin yin haka, gama ya zama kamar bashi ne a
gare su. Da yake Al'ummai sun sami rabo cikin albarkun ruhaniyar Yahudawa, ya

† **15:9** 2Sam 22.50; Zab 18.49 ‡ **15:10** M Sh 32.43 § **15:11** Zab 117.1 * **15:12** Ish 11.10 † **15:21** Ish 52.15

zama musu kamar bashi su ma su taimaki Yahudawa da albarkunsu na kayan duniya.
28 Saboda haka in na kammala wannan aiki na kuma tabbata cewa sun karɓi wannan
amfani, zan tafi Sifen in kuma ziyarce ku a hanyata. 29 Na san cewa sa'ad da na zo
wurinku, zan zo ne cikin yalwar albarkar Kiristi.

30 Ina roƙonku 'yan'uwa, saboda Ubangijinmu Yesu Kiristi da kuma saboda ƙaunar
Ruhu, ku haɗa kai tare da ni cikin famata ta wurin yin addu'a ga Allah saboda
ni. 31 Ku yi addu'a don in kuɓuta daga hannun marasa bi a Yahudiya don kuma
gudummawar da nake kaiwa Urushalima ta zama abar karɓa ga tsarkaka a can,
32 don da yardar Allah, in iso wurinku da farin ciki in kuma wartsake tare da ku.
33 Allah na salama yǎ kasance tare da ku duka. Amin.

# 16

*Gaisuwa ta kaina*

1 Ina gabatar muku da 'yar'uwarmu Fibi, baranyar ikkilisiya a Kenkireya. 2 Ina
roƙonku ku karɓe ta a cikin Ubangiji yadda ya dace a karɓi tsarkaka a kuma ba
ta kowane irin taimakon da take bukata daga wurinku, gama ta zama mai taimako
ƙwarai ga mutane masu yawa, haɗe da ni ma.

3 Ku gai da Firiskila da Akwila, abokan aikina cikin Kiristi Yesu. 4 Sun yi kasai
da ransu saboda ni. Ba ni kaɗai nake musu godiya ba amma har ma da dukan
ikkilisiyoyin Al'ummai.

5 Ku kuma gai da ikkilisiyar da take haɗuwa a gidansu.

Ku gai da ƙaunataccen abokina Efenetus, wanda ya zama na farko a karɓar Kiristi
a lardin Asiya.

6 Ku gai da Maryamu wadda ta yi muku aiki tuƙuru.

7 Ku gai da Anduronikus da Yuniyas, dangina waɗanda aka daure a kurkuku tare
da ni. Su fitattu ne sosai a cikin manzanni, sun riga ni zama masu bin Kiristi.

8 Ku gai da Amfiliyatus, ƙaunataccena a cikin Ubangiji.

9 Ku gai da Urbanus, abokin aikinmu cikin Kiristi, da kuma ƙaunataccen abokina
Sitakis.

10 Ku gai da Afelles wanda amincinsa cikin Kiristi tabbatacce ne.

Ku gai da iyalin gidan Aristobulus.

11 Ku gai da ɗan'uwana, Hirodiyon.

Ku gai da iyalin gidan Narkissus da suke cikin Ubangiji.

12 Ku gai da Tiryifena da Tiryifosa, matan nan da suke aiki tuƙuru cikin Ubangiji.

Ku gai da ƙaunatacciyata Fersis, wata matan da ta yi aiki tuƙuru cikin Ubangiji.

13 Ku gai da Rufus zaɓaɓɓe cikin Ubangiji, da kuma mahaifiyarsa, wadda ta zama
kamar mahaifiya a gare ni.

14 Ku gai da Asinkiritus, Filegon, Hermes, Faturobas, Hermas da kuma 'yan'uwan
da suke tare da su.

15 Ku gai da Filologus, Yuliya, Nereyus da 'yar'uwarsa, da kuma Olimfas da dukan
tsarkakan da suke tare da su.

16 Ku gaggai da juna da sumba mai tsarki.

Dukan ikkilisiyoyin Kiristi suna gaishe ku.

17 Ina roƙonku, 'yan'uwa, ku yi hankali fa da masu raba tsakani, saɓanin koyarwar
da kuka koya, suna sa tuntuɓe. Ku yi nesa da su. 18 Gama irin waɗannan mutane
ba sa bautar Ubangijinmu Kiristi, sai dai cikinsu. Ta wurin yaudara da kuma daɗin
baki, suna ruɗin marasa wayo. 19 Kowa ya riga ya ji game da biyayyarku, don haka

ina cike da farin ciki game da ku; amma ina so ku zama masu hikima game da abin
da yake nagari, ku kuma zama marasa laifi ga abin da yake mugu.

20 Allah na salama zai tattake Shaiɗan ba da daɗewa ba yă kuma sa shi a ƙarƙashin
sawunku.

Alherin Ubangijinmu Yesu kuma yă kasance tare da ku.

21 Timoti, abokin aikina, yana gai da ku, haka ma Lusiyus, Yason, da Sosifater,
dangina.
22 Ni, Tertiyus, wanda ya rubuta wannan wasiƙa, ina gai da ku cikin Ubangiji.
23 Gayus, mai masauƙina, mai kuma saukar da dukan 'yan Ikkilisiya, yana gaishe
ku.
Erastus, mai bi da ayyukan jama'ar gari, da kuma ɗan'uwanmu Kwartus, suna
gaishe ku.*

25 Daukaka ta tabbata ga mai ikon ƙarfafa ku bisa ga bisharata, bisa ga wa'azin Yesu
Kiristi, wadda ta gare ta ne aka bayyana asirin nan da yake ɓoye tun fil azal, 26 amma
yanzu kuwa aka bayyana, aka kuma sanar ta wurin rubuce-rubucen annabawa bisa
ga umarnin Allah madawwami, domin dukan al'ummai su gaskata su kuma yi masa
biyayya 27 ɗaukaka ta tabbata har abada ga Allah, wanda shi ne kaɗai mai hikima ta
wurin Yesu Kiristi! Amin.

* **16:23** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da gaisuwarsu. 24 Alherin Ubangijinmu Yesu Almasihu yă tabbata a gare ku duka. Amin

# 1 Korintiyawa

[1] Bulus, wanda aka kira domin yă zama manzon Kiristi Yesu, bisa ga nufin Allah, da kuma ɗan'uwanmu Sostenes,

[2] Zuwa ga ikkilisiyar Allah da take a Korint, da waɗanda aka tsarkake cikin Kiristi Yesu, aka kuma kira domin su zama masu tsarki, tare da dukan waɗanda suke ko'ina da suke kiran sunan Ubangijinmu Yesu Kiristi, Ubangijinsu da kuma namu.

[3] Alheri da salama daga Allah Ubanmu, da Ubangiji Yesu Kiristi, su kasance tare da ku.

### *Godiya*

[4] Ina gode wa Allah kullum dominku, saboda alherinsa da aka ba ku a cikin Kiristi
Yesu. [5] Gama a cikinsa kuka sami wadata ta kowace hanya, a cikin dukan maganarku,
da kuma cikin dukan saninku [6] gama shaidarmu game da Kiristi ta tabbata a cikinku.
[7] Saboda haka, ba ku rasa kowace baiwa ta ruhaniya ba, yayinda kuke jira da
marmari, saboda bayyanuwar Ubangijinmu Yesu Kiristi. [8] Zai ƙarfafa ku har zuwa
ƙarshe, domin ku zama marasa aibi a ranar Ubangijinmu Yesu Kiristi. [9] Allah, wanda
ya kira ku zuwa ga zumunci tare da Ɗansa Yesu Kiristi Ubangijinmu, shi mai aminci
ne.

### *Tsattsaguwa cikin ikkilisiya*

[10] Ina roƙonku 'yan'uwa, a cikin sunan Ubangijinmu Yesu Kiristi, dukanku ku yarda
da juna, domin kada a sami tsattsaguwa a cikinku, domin kuma ku zama ɗaya,
cikakku a cikin halinku da tunaninku. [11] 'Yan'uwana, waɗansu daga iyalin gidan
Kulos sun gaya mini cewa, akwai faɗa a cikinku. [12] Abin da nake nufi shi ne, ɗaya
daga cikinku na cewa, "Ni ina bin Bulus," wani na cewa, "Ni ina bin Afollos," wani
kuma, "Ni ina bin Kefas," har wa yau wani kuma, "Ni ina bin Kiristi."
[13] Kiristi a rabe ne? Bulus ne aka gicciye dominku? An yi muku baftisma a cikin
sunan Bulus ne? [14] Ina godiya domin ban yi wa wani baftisma a cikinku ba, sai dai
Kirisbus da Gayus kaɗai. [15] Don haka, ba wanda na iya cewa an yi muku baftisma
a cikin sunana. [16] (I, na kuma yi wa iyalin gidan Istifanas baftisma, ban da wannan,
ban tuna da wani da na yi masa baftisma ba.) [17] Gama Kiristi bai aike ni yin baftisma
ba, sai dai wa'azin bishara ba da kalmomin hikimar mutum ba, domin kada gicciyen
Kiristi ya rasa ikonsa.

### *Kiristi hikima da kuma ikon Allah*

[18] Gama saƙon gicciye wauta ne ga waɗanda suke hallaka, amma a gare mu, mu
da ake ceto, ikon Allah ne. [19] Gama a rubuce yake cewa,
"Zan rushe hikimar mai hikima,
basirar mai azanci kuma zan rikita shi."*
[20] Ina mai hikima? Ina mai zurfin bincike? Ina masana na wannan zamani? Ashe,
Allah bai wofinta hikimar duniya ba? [21] Gama tun da a cikin hikimar Allah, duniya a
cikin hikimarta ba tă san shi ba, Allah ya ji daɗin ceton waɗanda suka ba da gaskiya
ta wurin wautar wa'azin bishara. [22] Yahudawa suna so su ga alama, Hellenawa
kuma suna neman hikima, [23] amma mu, muna wa'azin Kiristi wanda aka gicciye ne,
wanda ya zama dutsen tuntuɓe ga Yahudawa, wauta kuma ga Al'ummai, [24] amma ga
su waɗanda Allah ya kira, Yahudawa da Hellenawa, Kiristi ikon Allah ne, da kuma

---
* **1:19** Ish 29.14

hikimar Allah. 25 Gama wautar Allah ta fi hikimar mutum, kuma rashin ƙarfin Allah
ya fi ƙarfin mutum.
26 ʼYanʼuwa, ku tuna yadda kuke saʼad da aka kira ku. Babu masu hikima da yawa
a cikinku, bisa ga ganin mutum; babu masu iko da yawa, babu masu martaba da
yawa bisa ga haihuwa. 27 Amma Allah ya zaɓi abubuwa masu wautata duniya, don
yă kunyata masu hikima. Allah ya zaɓi abubuwa marasa ƙarfi na duniya, domin ya
ba wa masu ƙarfi kunya. 28 Ya zaɓi abubuwa marasa martaba na wannan duniya da
kuma abubuwan da aka rena da abubuwan da ba a ɗauka a bakin kome ba, domin
a wofinta abubuwan da ake ganinsu da daraja, 29 domin kada wani ya yi taƙama a
gabansa. 30 Saboda Allah ne kuke cikin Kiristi Yesu, shi wanda ya zama hikima a gare
mu daga Allah. Kiristi shi ne adalcinmu, da tsarkinmu, da kuma fansarmu. 31 Saboda
haka, kamar yadda yake a rubuce cewa, "Duk wanda yake taƙama, ya yi taƙama a
cikin Ubangiji."†

# 2

1 Da na zo wurinku ʼyanʼuwa, ban zo da iya magana ko wani mafificin hikima
yayinda na yi muku shelar shaida game da Allah ba. 2 Don na ƙudura a raina saʼad da
nake tare da ku cewa ba zan mai da hankali ga kome ba sai dai Yesu Kiristi wanda aka
gicciye. 3 Na zo wurinku cikin rashin ƙarfi da tsoro, da rawan jiki ƙwarai. 4 Saƙona
da waʼazina ba su zo cikin hikima da kalmomin lallashi ba, sai dai da nuna ikon
Ruhu, 5 domin kada bangaskiyarku ta dogara a kan hikimar mutane, sai dai a kan
ikon Allah.

### *Hikima daga Ruhu*

6 Duk da haka, muna sanar da saƙon hikima cikin waɗanda suka balaga, amma
ba hikima irin ta wannan zamani ba ne, ko kuwa irin ta masu mulkin zamanin nan,
waɗanda za su shuɗe ba. 7 Aʼa, muna magana ne a kan asirin hikimar Allah, hikimar
da tun dā, take a ɓoye, wadda Allah ya ƙaddara domin ɗaukakarmu, tun kafin farkon
zamanai. 8 Ba ko ɗaya daga cikin masu mulkin wannan zamani da ya fahimce ta,
gama da a ce sun fahimce ta, da ba su gicciye Ubangiji mai ɗaukaka ba. 9 Duk da
haka, kamar yadda yake a rubuce cewa,
"Ba idon da ya taɓa gani,
ba kunnen da ya taɓa ji,
ba kuma zuciyar da ta taɓa tunanin
abin da Allah ya shirya wa masu ƙaunarsa."*
10 Amma Allah ya bayyana mana shi ta wurin Ruhunsa.
Ruhu yana bincika dukan abubuwa, har ma da abubuwa masu zurfi na Allah.
11 Wane ne a cikin mutane ya san tunanin mutum, in ba ruhun mutumin da yake
cikinsa ba? Haka kuma ba wanda ya san tunanin Allah, sai dai Ruhun Allah. 12 Ba
mu karɓi ruhun duniya ba, sai dai Ruhun da yake daga Allah, domin mu fahimci
abin da Allah ya ba mu hannu sake. 13 Wannan shi ne abin da muke sanarwa, ba da
kalmomin da muka koya ta wurin hikimar mutum ba, amma da kalmomin da Ruhu
yake koyarwa, muna faɗin gaskiya ta ruhaniya da kalmomin ruhaniya. 14 Mutumin
da ba shi da Ruhu, ba ya yarda da abubuwan da suka fita daga Ruhun Allah, domin
wauta ce a gare shi. Ba kuwa zai fahimce su ba, domin ta Ruhu ne ake fahimtarsu.
15 Mutumin ruhaniya yakan gwada dukan abubuwa, amma shi kansa ba ya ƙarƙashin
shariʼar mutum.
16 "Wa ya taɓa sanin hankalin Ubangiji,
har da zai koya masa?"†
Amma muna da tunani iri na Kiristi ne.

---

† **1:31** Irm 9.24 * **2:9** Ish 64.4 † **2:16** Ish 40.13

# 3

*A kan tsattsaguwa a cikin ikkilisiya*

1 ’Yan’uwa, ban iya yi muku magana kamar masu ruhaniya ba, sai dai kamar masu
halin mutuntaka, jarirai cikin bin Kiristi kawai. 2 Na ba ku madara ba abinci mai
tauri ba, domin ba ku balaga ba a lokacin. Kai, har yanzu ma, ba ku balaga ba. 3 Har
yanzu kuna rayuwa bisa ga halin mutuntaka. Da yake akwai kishi da faɗace-faɗace
a cikinku, ba rayuwa irin ta halin mutuntaka ke nan kuke yi ba? Kuma ba rayuwa
irin ta mutane ce kawai kuke yi ba? 4 Gama sa’ad da wani ya ce, “Ni na Bulus ne,”
wani kuma ya ce, “Ni na Afollos ne,” ba rayuwa irin ta mutane ke nan kuke yi ba?
5 Shin, wane ne Afollos? Wane ne kuma Bulus? Ai, bayi ne kawai waɗanda ta
wurinsu kuka gaskata, kamar yadda Ubangiji ya ba kowannensu aikinsa. 6 Ni na
shuka iri, Afollos kuma ya yi banruwa, amma Allah ne ya sa irin ya yi girma. 7 Don
haka, da wanda ya yi shuki, da wanda ya yi banruwa, ba a bakin kome suke ba, sai
dai Allah kaɗai, mai sa abubuwa su yi girma. 8 Mutumin da ya yi shuki, da mutumin
da ya yi banruwa nufinsu ɗaya ne, kuma kowannensu zai sami lada gwargwadon
aikinsa. 9 Gama mu abokan aiki ne na Allah; ku kuwa gonar ce ta Allah, ginin Allah
kuma.
10 Ta wurin alherin da Allah ya ba ni, na kafa tushen gini kamar ƙwararren magini,
wani kuma dabam yana gini a kai. Amma kowa yǎ lura da yadda yake gini. 11 Gama
babu wanda zai iya kafa wani tushen gini dabam da wanda aka riga aka kafa, wanda
yake Yesu Kiristi. 12 In wani ya yi gini a kan tushen ginin nan da zinariya, azurfa,
duwatsu masu daraja, itace, ciyawa ko kara, 13 aikin zai bayyana kansa, domin za a
nuna shi a sarari a Ranar. Wuta ce za tǎ bayyana aikin, wutar kuwa za tǎ gwada
ingancin aikin kowa. 14 In abin da kowane mutum ya gina ya tsaya, zai sami lada.
15 In ya ƙone, zai yi hasara, amma zai sami ceto, sai dai kamar wanda ya bi ta tsakiyar
wuta ne.
16 Ashe, ba ku sani ba cewa ku kanku haikalin Allah ne, Ruhun Allah kuma yana
zaune a cikinku? 17 Duk wanda ya ɓata haikalin Allah, Allah zai ɓata shi, don haikalin
Allah mai tsarki ne, ku ne kuwa haikalin nan.
18 Kada ku ruɗi kanku. In waninku yana tsammani cewa yana da hikima, yadda
duniya ta ɗauki hikima, to, sai ya mai da kansa “wawa” don yǎ zama mai hikima.
19 Gama hikimar duniyan nan, wauta ce a gaban Allah, kamar yadda yake a rubuce
cewa, “Yakan kama masu hikima a cikin makircinsu”*; 20 kuma a rubuce yake cewa,
“Ubangiji ya san dukan tunanin masu hikima banza ne.” 21 Saboda haka, kada wani
yǎ yi taƙama da mutum! Gama kome naku ne, 22 ko Bulus ko Afollos ko Kefas ko
duniya ko rai ko mutuwa ko abubuwa na yanzu ko na nan gaba, ai, duka naku ne,
23 ku kuwa na Kiristi ne, Kiristi kuma na Allah ne.

# 4

*Manzannin Kiristi*

1 Saboda haka, ya kamata mutane su ɗauke mu a matsayin bayin Kiristi, da kuma a
matsayin waɗanda aka ba su amanar asirin abubuwan Allah. 2 Yanzu fa, ana bukatar
waɗanda aka ba su riƙon amana, dole su zama masu aminci. 3 Karamin abu ne a
gare ni a ce ku ne za ku gwada ni, ko kuwa a gwada ni a wata kotun mutane, ai, ko
ni kaina ba na yanka wa kaina hukunci. 4 Lamirina bai ba ni laifi ba, sai dai wannan
bai mai da ni marar laifi ba. Ubangiji ne mai hukunta ni. 5 Saboda haka, kada ku
shari’anta kome tun lokaci bai yi ba. Ku jira sai Ubangiji ya zo. Zai bayyana abin da
yake a ɓoye a cikin duhu a sarari, zai kuma tone nufin zukatan mutane. A lokacin
ne fa kowa zai karɓi yabo daga wurin Allah daidai gwargwado.

* **3:19** Ayu 5.13

6 To, fa ’yan’uwa, ga zancen waɗannan abubuwa, na misalta su ne ga kaina, da
kuma Afollos saboda ku, don ku yi koyi da mu a kan abin da ake nufi da cewa, “Kada
ku zarce abin da yake a rubuce.” Ta haka, ba za ku yi taƙama da wani mutum fiye
da wani ba. 7 Wa ya ce ka fi sauran mutane? Me kuma kake da shi, wanda ba karɓa
ka yi ba? In kuma karɓa ka yi, me ya sa kake taƙama kamar ba karɓa ba ne ka yi?
8 Kun riga kun sami duk abin da kuke nema! Kun riga kun yi arziki! Kun zama
sarakuna, kun kuma zama haka ɗin ba tare da mu ba! Da a ce kun riga kun zama
sarakuna mana da sai mu zama sarakuna tare da ku! 9 Gama a ganina fa, Allah ya
baje mu manzanni a ƙarshen jerin gwanon, a matsayin mutanen da aka hukunta ga
mutuwa a filin wasanni. Mun zama abin kallo ga dukan duniya, ga mala’iku da kuma
mutane. 10 Mun zama masu wauta saboda Kiristi, ku kuwa kuna da hikima sosai a
cikin Kiristi! Ba mu da ƙarfi, amma ku kuna da ƙarfi! Ana girmama ku, mu kuwa
ana ƙasƙantar da mu! 11 Har yă zuwa wannan sa’a, yunwa da ƙishirwa muke ciki,
muna sanye da tsummoki, ana wulaƙanta mu, ba mu kuma da gida. 12 Muna aiki
da gaske da hannuwanmu. In aka la’anta mu, mukan sa albarka. In aka tsananta
mana, mukan jimre; 13 in aka ɓata mana suna, mukan mayar da alheri. Har yă zuwa
wannan lokaci, mu ne kamar jujin duniya, abin ƙyamar kowa.
14 Ba don in kunyata ku ba ne na rubuta wannan, sai dai don in gargaɗe ku a
kan cewa ku ’ya’yana ne, ƙaunatattu. 15 Ko da kuna da iyayen riƙo dubu goma
cikin Kiristi, ba ku da ubanni da yawa, gama a cikin Kiristi Yesu, na zama mahaifi a
gare ku, ta wurin bishara. 16 Saboda haka, ina roƙonku ku yi koyi da ni. 17 Saboda
wannan dalili ina aika muku Timoti, ɗana, wanda nake ƙauna, mai aminci kuma a
cikin Ubangiji. Zai tunashe ku game da yadda za ku bi Kiristi Yesu da kuma yadda
ya yi daidai da yadda nake koyarwa a ko’ina, a kowace ikkilisiya.
18 Waɗansunku suna tsammani ba zan zo wurinku ba har suna ɗagankai. 19 Amma
in Ubangiji ya yarda zan zo wurinku ba da daɗewa ba. Sa’an nan zan bincike ko masu
wannan yawan ɗagan kan nan suna da wani iko. 20 Gama mulkin Allah ba cika baki
ba ne, sai dai ga iko. 21 Wanne kuka fi so in na zo? Kuna so in tsananta muku ko in
zama mai hankali da kuma sauƙinkai?

# 5

*A yi waje da ɗan’uwa mai halin lalata*

1 Ana ba da labari cewa ana lalata a cikinku, irin da ba a ma samu a cikin masu
bautar gumaka. Har mutum yana kwana da matar mahaifinsa. 2 Har ya zama muku
abin taƙama! Ashe, bai kamata ku cika da baƙin ciki ku kuma daina zumunci da
mutumin da yake aikata wannan ba? 3 Ko da yake ba na nan tare da ku cikin jiki,
ina tare da ku a cikin ruhu. Na riga na yanke wa wanda ya aikata wannan hukunci,
kamar dai ina tare da ku. 4 Saboda haka sa’ad da kun taru ikon Ubangijinmu Yesu
kuma yana nan, ni ma ina tare da ku. 5 Ku miƙa irin wannan mutum ga Shaiɗan, don
a hallaka halin nan na mutuntaka, ruhunsa kuma yă sami ceto a ranar da Ubangiji
zai dawo.
6 Ku daina taƙama. Ba ku san cewa ɗan ƙanƙanin yisti ne yakan sa dukan curin
burodi yă kumbura ba? 7 Ku kawar da tsohon yisti don ku zama kamar sabon
curi da aka yi babu yisti yadda dai kuke. Gama an miƙa Kiristi Ɗan Ragon Bikin
Ketarewarmu. 8 Saboda haka, sai mu kiyaye Bikin ba da burodi mai tsohon yisti ba,
ba kuma da yisti na ƙeta da mugunta ba, sai dai da burodi marar yisti na sahihanci
da na gaskiya.
9 Na rubuta muku cikin wasiƙata, kada ku yi haɗa kai da masu aikin lalata. 10 Ko
kusa, ba na nufin fasikai marasa bi, ko makwaɗaita da mazambata, ko matsafa, don
in haka ne, sai yă zama dole ku fita daga duniya. 11 Yanzu dai ina rubuta muku

cewa kada ku haɗa kai da duk mai kiran kansa ɗan'uwa, amma yana fasikanci, ko kwaɗayi, ko bautar gumaka, ko ɓata suna, ko mashayi, ko mazambaci. Kada ku ko ci abinci da irin wannan mutum. [12] Me zai kai yin hukunci ga waɗanda ba 'yan ikkilisiya ba. Ai, waɗanda suke 'yan ikkilisiya ne za ku hukunta. [13] Allah zai hukunta waɗanda ba namu ba. "Ku yi waje da irin mugun mutumin nan daga cikinku."*

# 6

*Kaiwa juna kotu*

[1] In wani a cikinku yana da damuwa da wani, don me zai kai ƙara a gaban marasa
bi, maimakon yă kai ƙara a gaban tsarkaka? [2] Ba ku san cewa tsarkaka ne za su yi
wa duniya shari'a ba? In kuwa za ku yi wa duniya shari'a, ai, kun isa ku yi shari'a
a kan ƙananan damuwoyi ke nan. [3] Ba ku san cewa za mu yi wa mala'iku shari'a
ba? Balle al'amuran da suka shafi duniyan nan! [4] Saboda haka, in kuna da damuwa
game da irin waɗannan al'amura, sai ku naɗa alƙalai ko cikin waɗanda ba kome ba
ne a ikkilisiya! [5] Na faɗi haka ne don ku ji kunya. Ashe, ba za a iya samun wani a
cikinku mai hikima wanda zai iya sasanta tsakanin masu bi ba? [6] Me zai sa ɗan'uwa
yă kai ƙarar ɗan'uwa, a gaban marasa bi?
[7] Karar junanku ma da kuke yi, ai, kāsawa ce a gare ku. Ba gara ku haƙura a cuce
ku ba? Ku kuma haƙura ko an zambace ku? [8] Amma ga shi ku da kanku kuna cuta,
kuna kuma zamba, har ma ga 'yan'uwanku ne kuke yi wannan. [9] Ba ku sani ba cewa
mugaye ba za su gāji mulkin Allah ba? Kada fa a ruɗe ku. Ba masu fasikanci ko masu
bautar gumaka ko masu zina ko karuwan maza, ko 'yan daudu, [10] ko ɓarayi ko masu
kwaɗayi ko mashaya ko masu ɓata suna ko masu zamba da za su gāji mulkin Allah.
[11] Haka waɗansu a cikinku ma suke a dā. Amma an wanke ku, an tsarkake ku, aka
kuma sa kuka zama marasa laifi cikin sunan Ubangijinmu Yesu Kiristi da kuma ta
wurin Ruhun Allahnmu.

*Fasikanci*

[12] "Ina da dama in yi kome," sai dai ba kome ba ne yake da amfani. "Ina da dama
in yi kome" sai dai ba abin da zai mallake ni. [13] "An yi abinci domin ciki ne, ciki
kuma domin abinci." Amma Allah zai hallaka su duka. Ba a yi jiki saboda fasikanci
ba, sai dai domin Ubangiji, Ubangiji kuma domin jiki. [14] Ta wurin ikonsa, Allah
ya tashe Ubangiji daga matattu, haka zai tashe mu mu ma. [15] Ba ku sani ba cewa
jikunanku gaɓoɓin Kiristi ne kansa? Zai kyautu in ɗauki gaɓoɓin Kiristi in haɗa da
jikin karuwa? Sam! [16] Ba ku san cewa shi wanda ya haɗa jikinsa da karuwa sun zama
ɗaya a cikin jiki ke nan ba? Gama an ce, "Biyun za su zama jiki ɗaya."* [17] Wanda
kuwa ya haɗa jikinsa da Ubangiji ya zama ɗaya da shi ke nan a ruhu.
[18] Ku guji fasikanci. Duk sauran zunubai da mutum yakan aikata suna waje da
jikinsa, amma mai yin fasikanci, yana ɗaukar alhalin jikinsa ne. [19] Ba ku san cewa
jikin nan naku haikalin Ruhu Mai Tsarki ba ne wanda yake cikinku yake kuma daga
Allah? Ku ba na kanku ba ne; [20] saye ku fa aka yi da tsada, saboda haka, sai ku
girmama Allah da jikinku.

# 7

*Aure*

[1] To, game da zancen da kuka rubuto. Yana da kyau mutum yă zauna ba aure.*
[2] Amma da yake fasikanci ya yi yawa, ya kamata kowane mutum yă kasance da
matarsa, kowace mace kuma da mijinta. [3] Ya kamata miji yă cika hakkinsa na aure ga

---

* **5:13** M Sh 17.7; M Sh 19.19; M Sh 21.21; M Sh 22.21,24; M Sh 24.7 * **6:16** Far 2.24 * **7:1** Ko kuwa "Ya fi kyau kada mutum yă yi jima'i da mace."

matarsa. Haka kuma matar ta yi ga mijinta. 4 Jikin matar ba nata ne kaɗai ba, amma
na mijinta ne ma. Haka ma jikin mijin, ba na shi ne kaɗai ba, amma na matarsa ne
ma. 5 Kada ku ƙi kwana da juna sai ko kun yarda a junanku kuma na ɗan lokaci, don
ku himmantu ga addu'a. Sa'an nan ku sāke haɗuwa don kada Shaiɗan yă jarrabce
ku saboda rashin ƙamewarku. 6 Wannan fa shawara ce nake ba ku, ba umarni ba.
7 Da ma a ce dukan maza kamar ni suke mana. Sai dai kowa da irin baiwar da Allah
ya yi masa; wani yana da wannan baiwa, wani kuwa wancan.

8 To, ga marasa aure da gwauraye kuwa ina cewa yana da kyau su zauna haka ba
aure, yadda nake. 9 Sai dai in ba za su iya ƙame kansu ba, to, su yi aure, don yă fi
kyau a yi aure, da sha'awa ta sha kan mutum.

10 Ga waɗanda suke da aure kuwa ina ba da wannan umarni (ba ni ba, amma
Ubangiji) cewa kada mace ta rabu da mijinta. 11 In kuwa ta rabu da shi, sai ta kasance
ba aure, ko kuma ta sāke shiryawa da mijinta. Kada miji kuma yă saki matarsa.

12 Ga sauran kuwa (ni ne fa na ce ba Ubangiji ba), in wani ɗan'uwa yana da mata
wadda ba mai bi ba ce, kuma tana so ta zauna tare da shi, kada yă sake ta. 13 In kuma
mace tana da miji wanda ba mai bi ba ne, kuma yana so yă zauna tare da ita, kada tă
kashe auren. 14 Don miji marar ba da gaskiya an tsarkake shi ta wurin matarsa. Mace
marar ba da gaskiya kuma an tsarkake ta ta wurin mijinta. In ba haka ba 'ya'yanku
ba za su zama da tsarki ba, amma kamar yadda yake, su masu tsarki ne.

15 Amma in marar bi ɗin ya raba auren, a ƙyale shi. A irin wannan hali, babu tilas
a kan wani, ko wata mai bi. Allah ya kira mu ga zaman lafiya ne. 16 Ke mace, kin
sani ne, ko ke ce za ki ceci mijinki? Kai miji, ka sani ne, ko kai ne za ka ceci matarka?

17 Duk da haka, sai kowa yă kasance a rayuwar da Ubangiji ya sa shi da kuma
wanda Allah ya kira shi. Umarnin da na kafa a dukan ikkilisiyoyi ke nan. 18 In an
riga an yi wa mutum kaciya sa'ad da aka kira shi, to, kada yă zama marar kaciya. In
an kira mutum sa'ad da yake marar kaciya, to, kada a yi masa kaciya. 19 Kaciya ba
wani abu ba ne, rashin kaciya kuma ba wani abu ba ne. Kiyaye umarnin Allah shi
ne muhimmin abu. 20 Ya kamata kowa yă kasance a matsayin da yake ciki sa'ad da
Allah ya kira shi.

21 Kai bawa ne sa'ad da aka kira ka? Kada wannan yă dame ka, sai dai in kana iya
samun 'yanci, sai ka yi amfani da wannan dama. 22 Gama wanda yake bawa sa'ad da
Ubangiji ya kira shi, 'yantacce ne na Ubangiji; haka ma, wanda yake 'yantacce sa'ad
da aka kira shi, bawa ne na Kiristi. 23 Da tsada fa aka saye ku, kada ku zama bayin
mutane. 24 'Yan'uwa, a duk matsayin da mutum yake sa'ad da aka kira shi, sai yă
kasance haka a sabuwar dangantakarsa da Allah.

25 To, game da budurwai. Ba ni da wani umarni daga Ubangiji, sai dai na yanke
hukunci a matsayi wanda yake amintacce ta wurin jinƙan Ubangiji. 26 Saboda ƙuncin
rayuwar da ake ciki, ina gani ya fi kyau ku kasance yadda kuke. 27 In kuna da aure,
kada ku nemi kashe auren. In ba ku da aure, kada ku nemi yin aure. 28 Amma idan
ka riga ka yi aure, to, ba laifi, ba zunubi ba ne, kuma idan yarinya† ta yi aure, ba
tă yi laifi ba. Sai dai waɗanda suka yi aure za su fuskanci damuwoyi masu yawa a
cikin rayuwa, ni kuwa ina so in fisshe su daga wannan.

29 'Yan'uwa, abin da nake nufi shi ne, lokaci ya rage kaɗan. Daga yanzu, waɗanda
suke da mata ya kamata su yi rayuwa kamar ba su da su; 30 waɗanda suke kuka
kuma kamar ba kuka suke yi ba, waɗanda suke farin ciki kuwa kamar ba farin ciki
suke yi ba. Waɗanda suka sayi abu su yi kamar ba nasu ba ne; 31 masu amfani da
kayan duniya kuwa, kada su duƙufa a cikinsu. Gama duniyan nan a yadda take mai
shuɗewa ce.

† **7:28** yarinya. Da Girik an rubuta “budurwa” ne nan

32 Zan so ku ʼyantu daga damuwa. Mutum marar aure ya damu ne da alʼamuran
Ubangiji, yadda zai gamshi Ubangiji. 33 Amma mutumin da yake da aure yakan damu
ne da alʼamuran wannan duniya, yadda zai gamshi matarsa 34 hankalinsa a rabe yake.
Mace marar aure ko kuwa budurwa ta damu ne da alʼamuran Ubangiji. Nufinta shi
ne ta ba da kanta ga Ubangiji cikin jiki da ruhu. Amma mace da take da aure ta damu
ne da alʼamuran wannan duniya, yadda za tă gamshi mijinta. 35 Na faɗa haka don
amfaninku ne, ba don in ƙuntata muku ba. Sai dai don ku yi rayuwa a hanyar da ta
dace da nufin ku himmantu ga bautar Ubangiji ba da raba hankali ba.
36 In mutum ya ga cewa ba ya nuna halin da ya kamata ga budurwar da ya yi
alkawarin aure da ita, in kuma shekarunta suna wucewa, shi kuma ya ga ya kamata
yă yi aure, to, sai yă yi. Ba zunubi ba ne. Ya kamata su yi aure. 37 Amma mutumin da
ya riga ya yanke shawara a ransa, wanda kuma ba lalle ba ne amma yana iya shan
kan nufinsa, kuma ya riga ya zartar a zuciyarsa ba zai auri budurwar ba, wannan
mutum ma ya yi abin da ya dace. 38 Don haka, wanda ya auri budurwar ya yi daidai,
amma wanda bai aure ta ba ya ma fi.‡
39 Mace tana haɗe da mijinta muddin yana da rai. Amma in mijinta ya mutu, tana
da ʼyanci ta auri wanda take so. Amma fa, sai mai bin Ubangiji. 40 A nawa raʼayi,
za tă fi jin daɗi in ta zauna haka, a ganina kuwa ina ba ku shawara ce daga Ruhun
Allah da na ce haka.

# 8

*Abincin da aka miƙa wa gumaka*

1 To, game da abincin da aka miƙa hadaya ga gumaka kuwa. Mun san cewa
dukanmu muna da ilimi. Ilimi yakan kawo girman kai, amma ƙauna takan gina.
2 Mutumin da yake tsammani ya san abu, sanin da yake da shi bai isa ba. 3 Amma
mutumin da yake ƙaunar Allah, Allah yana sane da shi.
4 To, game da cin abincin da aka miƙa hadaya ga gumaka kuwa, mun san cewa
"Gunki ba kome ba ne a duniya", kuma "Babu wani Allah sai dai ɗaya." 5 Gama ko
da akwai abubuwan da ake ce da su alloli, a sama ko a ƙasa (don kuwa akwai "alloli"
da "iyayengiji" da yawa), 6 duk da haka a gare mu dai akwai Allah ɗaya kaɗai, Uba,
wanda dukan abubuwa suke daga gare shi, wanda kuma saboda shi ne muke rayuwa,
kuma akwai Ubangiji ɗaya, Yesu Kiristi, wanda ta wurinsa ne aka yi dukan abu, ta
wurinsa ne kuma muke rayuwa.
7 Amma ba kowa ne ya san wannan ba. Har yanzu, waɗansu mutane sun saba da
tunani cewa gumaka ainihi ne, saboda haka saʼad da suka ci irin abincin nan, sukan
ɗauka cewa kamar an miƙa wa ga gunki ne, kuma da yake lamirinsu ba ƙarfi, yakan
ƙazantu. 8 Gaskiya ne cewa ba ma samun yardar Allah ta wurin abin da muke ci. Ba
ma rasa wani abu idan ba mu ci ba, kuma ba ma ƙaru da wani abu in muka ci.
9 Sai dai ku yi hankali, kada yin amfani da ʼyancinku yă zama abin sa tuntuɓe ga
marasa ƙarfi. 10 Gama in wani wanda lamirinsa ba shi da ƙarfi ya gan ka, kai da
kake da wannan sani, kana ci a haikalin gumaka, ashe, ba zai sami ƙarfin halin cin
abin da aka miƙa wa gumaka ba? 11 Saboda haka ta wurin sanin nan naka sai ka sa
wannan ɗanʼuwa marar ƙarfi wanda Kiristi ya mutu dominsa yă hallaka. 12 Saʼad da
ka rushe lamiri mai bi marar ƙarfi, ka yi wa Kiristi zunubi ke nan. 13 Saboda haka, in

‡ **7:38** Ko kuwa 36 In wani yana tsammani cewa ba ya yin wa ʼyarsa abin da ya dace, in kuma shekarunta suna ƙaruwa, ya kuwa ji ya kamata tă yi aure, sai yă yi yadda ya ga ya dace. Bai yi zunubi ba. Ya kamata yă bar ta tă yi aure. 37 Amma mutumin da ya warware batun a zuciyarsa, wanda ba ya ƙarƙashin tilas amma yana iya sarrafa nufinsa, wanda kuma ya yanke shawara yă bar budurwarsa ba aure, wannan mutum ma ya yi abin da yake daidai. 38 Saboda haka, wanda ya ba da budurwarsa a aure ya yi daidai, amma wanda bai ba da ita ga aure ba ya ma yi abin da ya fi.

abin da nake ci zai sa ɗan'uwana yǎ yi zunubi, ba zan ƙara cin nama ba, don kada
in sa shi yǎ yi tuntuɓe.

# 9

*Hakkin manzo*

1 Ba ni da 'yanci ne? Ni ba manzo ba ne? Ni ban gan Yesu Ubangijinmu ba ne? Ba ku
ne sakamakon aikina cikin Ubangiji ba? 2 Ko da waɗansu ba su ɗauke ni a matsayin
manzo ba, tabbatacce, ni manzo ne a gare ku! Gama ku ne hatimin manzancina a
gaban Ubangiji.
3 Wannan ita ce kāriyata ga waɗanda suke tuhumata game da manzancina. 4 Ba
mu da 'yancin ci da sha ne? 5 Ba mu da 'yancin tafiya tare da matar da muka aura
mai bi kamar sauran manzanni da 'yan'uwan Ubangiji da kuma Kefas suke yi? 6 Ko
ni da Barnabas ne kawai ba mu da 'yanci a ɗauke mana aikin ci da kai?
7 Wa yake ciyar da kansa yayinda yake aikin soja? Wa yake shukar gonar inabi,
da ba ya cin amfaninta? Wa yake kiwon garke, da ba ya sha madararsa? 8 Ina faɗin
wannan bisa ga ra'ayin mutum kawai ne? Ashe, Doka ma ba tǎ faɗa haka ba? 9 Gama
yana a rubuce a cikin Dokar Musa cewa, “Kada ka sa wa saniya takunkumi sa'ad da
yake sussukar hatsi.”* Kuna tsammani a kan shanu ne Allah ya damu sa'ad da ya
ce haka? 10 Babu shakka, ya yi maganan nan saboda mu ne. Ko ba haka ba? I, an
rubuta wannan saboda mu ne, domin sa'ad da mai noma yake noma, mai sussuka
kuma yana sussuka, suna wannan ne da bege za su sami rabonsu daga girbin. 11 In
muka shuka iri na ruhaniya a cikinku, ashe, bai kamata mu yi girbin abin biyan
bukatarmu daga gare ku ba? 12 In waɗansu suna samun wannan taimako daga gare
ku, ashe, mu ba mu fi cancanta mu samu ba?
Amma ba mu yi amfani da wannan 'yancin ba. A maimakon haka, mun jure da
kome, domin kada mu hana bisharar Kiristi yaɗuwa.
13 Ashe, ba ku san cewa waɗanda suke hidima a haikali suna samun abincinsu daga
haikali ba ne, waɗanda kuma suke hidima a bagade suna samun rabo a hadayar da
suka miƙa ba ne? 14 Haka ma Ubangiji ya umarta cewa ya kamata waɗanda suke
wa'azin bishara, su sami abin biyan bukatarsu daga bisharar.
15 Amma ban yi amfani da ko ɗaya daga cikin waɗannan 'yancin ba. Ba kuma ina
rubuta muku wannan da fata za ku yi mini waɗannan abubuwa ba ne. Gwamma
in mutu, da wani yǎ hana ni wannan abin taƙama. 16 Duk da haka, sa'ad da ina
wa'azin bishara, ba na taƙama, domin tilas ne a gare ni in yi wa'azi. Kaitona, in ban
yi wa'azin bishara ba! 17 In na yi wa'azi da yardar rai, ina da lada; in ba da yardar
rai ba, ina dai cika amana da aka danƙa mini ne. 18 To, mene ne ladana? Ladana
kaɗai shi ne, in yi wa'azin bishara, in kuma yi shi a kyauta, yadda ba zan yi amfani
da 'yancina cikin wa'azin ba.
19 Ko da yake ina da 'yanci ba na kuma ƙarƙashin kowa, na mai da kaina bawa ga
kowa, domin in rinjayi mutane da yawa. 20 Ga Yahudawa na zama kamar mutumin
Yahuda, domin in rinjayi Yahudawa. Ga waɗanda suke ƙarƙashin doka kuma, na
zama kamar wanda yake ƙarƙashin Dokar (ko da yake ni kaina ba na ƙarƙashin
Doka), domin in rinjayi waɗanda suke ƙarƙashin Doka. 21 Ga waɗanda ba su da
Dokar kuwa, na zama kamar wanda ba shi da Dokar (ko da yake ba ni da 'yanci daga
dokar Allah, amma ina ƙarƙashin dokar Kiristi), domin in rinjayi waɗanda ba su da
dokar. 22 Ga waɗanda ba su da ƙarfi, na zama marar ƙarfi, domin in rinjayi waɗanda
ba su da ƙarfi. Na zama dukan abu ga dukan mutane, domin ko ta yaya in zai yiwu,
in ceci waɗansu. 23 Ina yin dukan waɗannan ne saboda bishara, domin in sami rabo
a cikin albarkarta.

* **9:9** M Sh 25.4

[24] Ba ku sani ba cewa a gasar gudu, dukan masu gudu sukan yi gudu, amma guda
ne kaɗai yakan sami lada? To, sai ku yi gudu yadda za ku sami lada. [25] Duk ʼyan
wasan gasa sukan hori kansu sosai. Sukan yi haka domin su sami rawanin da ba zai
daɗe ba. Amma mu muna yi ne domin mu sami rawanin da zai dawwama. [26] To, ni
fa ba gudu nake yi kamar mai gudu ba wurin zuwa ba. Dambena kuma ba naushin
iska nake yi ba. [27] Aʼa, ina horon jikina in mai da shi bawana, saboda bayan na yi
wa waɗansu waʼazi, ni kaina kada in kāsa cancantar samun lada.

# 10

*Gargaɗi daga tarihin Israʼila*

[1] Ba na so ku kasance da rashin sani, ʼyanʼuwa, cewa dukan kakannin-kakanninmu
sun yi tafiya a ƙarƙashin girgije, dukansu kuma suka bi ta tsakiyar teku. [2] An yi wa
dukansu baftisma ga bin Musa a cikin girgije da kuma cikin teku. [3] Dukansu sun ci
abincin ruhaniya guda [4] suka kuma sha ruwan ruhaniyan nan guda; gama sun sha
daga dutsen ruhaniya nan, wanda ya yi tafiya tare da su, wannan dutsen kuwa Kiristi
ne. [5] Duk da haka, Allah bai ji daɗin yawancinsu ba; gawawwakinsu kuwa suka bazu
koʼina a cikin hamada.
[6] To, waɗannan abubuwa misalai* ne a gare mu, kada mu yi marmarin mugayen
abubuwa, kamar yadda suka yi. [7] Kada ku zama masu bautar gumaka, yadda
waɗansunsu suka zama; kamar yadda yake a rubuce cewa, "Mutanen suka zauna
don su ci su kuma sha, suka kuma tashi suka shiga rawa ta rashin kunya."† [8] Kada fa
mu yi fasikanci yadda waɗansunsu suka yi, har a rana guda mutane dubu ashirin da
uku a cikinsu suka mutu. [9] Kada mu gwada Kiristi yadda waɗansunsu suka yi, har
macizai suka kakkashe su. [10] Kada kuma ku yi gunaguni yadda waɗansunsu suka
yi, har malaʼika mai hallakarwa ya hallaka su. [11] Waɗannnan abubuwa sun same su
ne, domin su zama abubuwan koyi, aka kuma rubuta su domin a gargaɗe mu, mu
da ƙarshen zamani ya zo mana. [12] Saboda haka in kana tsammani kana tsaye ne, to,
ka yi hankali kada ka fāɗi! [13] Ba jarrabar da ta taɓa samunku, wadda ba a saba yi
wa mutum ba. Allah mai aminci ne; ba zai bari a jarrabce ku fiye da ƙarfinku ba.
Amma in aka jarrabce ku, zai nuna muku mafita, domin ku iya cin nasara.

*Bukukkuwan gumaka da cimar Ubangiji*

[14] Saboda haka abokaina ƙaunatattu, ku guje wa bautar gumaka. [15] Ina magana
da ku a kan ku mutane ne fa masu azanci; ku duba da kanku ku ga abin da nake
faɗa. [16] Kwaf nan na godiya da muke yin godiya da shi, ashe ba tarayya ce a cikin
jinin Kiristi ba? Wannan burodi kuma da muke karya mu ci, ashe, ba tarayya ne a
cikin jikin Kiristi ba? [17] Da yake burodin nan ɗaya ne, ashe kuwa, mu da muke da
yawa jiki ɗaya ne, gama dukanmu muna ci daga burodi nan guda.
[18] Ku dubi mutanen Israʼila mana. Ashe, waɗanda suke cin hadayu, ba ɗaya suke
da juna cikin cin hadayun da aka miƙa a bagade ba? [19] To, me kuke tsammani nake
nufi a nan? Hadayar da aka miƙa wa gunki ce wani abu, ko kuma gunkin ne wani
abu? [20] Aʼa, ina nufin akan miƙa hadayun da masu bautar gumaka suka wa aljanu
ne, ba Allah ba. Ba na so ku zama ɗaya da aljanu. [21] Ba zai yiwu ku sha daga kwaf na
Ubangiji ku kuma sha daga kwaf na aljanu ba, ba ya yiwuwa ku ci a teburin Ubangiji,
ku kuma ci a teburin aljanu. [22] Ashe, so muke mu tsokani Ubangiji ya yi kishi? Mun
fi shi ƙarfi ne?

*ʼYancin mai bi*

[23] "Ana da dama a yi kome" sai dai ba kome ba ne yake da amfani. "Ana da dama
a yi kome" sai dai ba kome ba ne mai ginawa. [24] Kada wani yǎ kula da kansa kawai,

---

* **10:6** Ko kuwa ire-ire; haka ma a aya 11 † **10:7** Fit 32.6

sai dai yă kula da waɗansu kuma. [25] Ku ci kowane abin da ake sayarwa a kasuwar
nama ba sai kun tambaya ba don kada lamiri yă damu da inda abin ya fito, [26] gama
"Duniya da duk abin da yake cikinta na Ubangiji ne."‡
[27] In wani marar bi ya gayyace ku cin abinci kuka kuwa yarda ku je, sai ku ci ko
mene ne da aka sa a gabanku, ba tare da tambaya don kada lamiri yă damu da inda
abin ya fito. [28] Sai dai in wani ya ce muku, "Ai, wannan an miƙa ne wa gunki," to,
kada ku ci, saboda duban mutuncin wannan da ya gaya muku, don kuma lamiri yă
kasance babu laifi [29] ina nufin lamirin wancan mutum ne fa, ba naku ba. Don me
lamirin wani zai shari'anta 'yancina? [30] In na ci abinci da godiya, don me za a zarge
ni a kan abin da na ci da godiya ga Allah?
[31] Saboda haka, duk abin da kuke yi, ko ci ko sha, ku yi shi duka saboda ɗaukakar
Allah. [32] Kada ku sa wani yă yi tuntuɓe, ko mutumin Yahuda ne, ko mutumin
Al'ummai ko kuma ikkilisiyar Allah [33] kamar dai yadda nake ƙoƙarin faranta wa
kowa rai, ta kowace hanya. Gama ba don kaina kaɗai nake yi ba, sai dai don amfanin
mutane da yawa, don su sami ceto.

# 11

[1] Ku bi gurbina, kamar yadda ni nake bin gurbin Kiristi.

### *Da'a cikin sujada*

[2] Ina yabonku saboda kuna tunawa da ni a cikin kowane abu, kuna kuma riƙe da
koyarwar,* yadda na ba ku. [3] To, ina so ku gane cewa shugaban kowane namiji Kiristi
ne, shugaban mace namiji ne, shugaban Kiristi kuma Allah ne. [4] Kowane namijin da
ya yi addu'a ko annabci da kansa a rufe ya jawo kunya wa kansa. [5] Duk macen da ta
yi addu'a ko annabci da kanta a buɗe kuwa ta rena kanta, ya zama kamar an aske
kanta ke nan. [6] In mace ba ta so tă rufe kanta, to, sai tă aske gashinta; in kuwa abin
kunya ne mace tă yanke ko tă aske gashinta, to, sai tă rufe kanta.
[7] Namiji kuwa bai kamata ya rufe kansa ba,† da yake shi kamannin Allah ne, da
kuma darajar Allah, amma mace dai, darajar namiji ne. [8] Gama namiji bai fito daga
mace ba, sai dai mace ce ta fito daga namiji. [9] Ba a kuma halicci namiji don mace
ba, sai dai mace don namiji. [10] Don haka, saboda wannan, da kuma saboda mala'iku,
dole mace ta ɗaura wani abu a kanta. [11] Duk da haka a cikin Ubangiji, mace ba a
rabe take da namiji ba, namiji kuma ba a rabe yake da mace ba. [12] Kamar yadda
mace ta fito daga namiji, haka kuma aka haifi namiji ta wurin mace. Sai dai kowane
abu daga Allah yake.
[13] Ku kanku duba mana. Ya yi kyau mace tă yi addu'a ga Allah da kanta a buɗe?
[14] Kai, yadda halitta take ma, ai, ta koya muku cewa in namiji yana da dogon gashi,
abin kunya ne a gare shi, [15] amma in mace tana da dogon gashi, ai, daraja ce a gare
ta. Gama an ba ta dogon gashi saboda rufe kanta ne. [16] In akwai mai gardama da
wannan, to, mu dai ba mu da wata al'ada, haka ma ikkilisiyoyin Allah.

### *Cimar Ubangiji*

[17] Game da umarnan nan dai, ban yaba muku ba, domin taruwarku ba ta kirki ba
ce, ɓarna ce. [18] Da farko dai, na ji cewa sa'ad da kuka taru a matsayin ikkilisiya,
akwai tsattsaguwa a tsakaninku, har na fara yarda da zancen. [19] Ba shakka dole a
sami bambanci a tsakaninku don a nuna wa Allah ya amince da shi a cikinku. [20] Sa'ad

‡ **10:26** Zab 24.1 * **11:2** Ko kuwa al'adu † **11:7** Ko kuwa 4 Duk namijin da ya yi addu'a ko annabci da dogon gashin kai, ya rena kansa. 5 Duk macen da ta yi addu'a ko annabci ba tare da ta rufe gashin kanta ba kuwa ta rena kanta, ta yi kama da ɗaya a cikin "matan da aka yi wa aski." 6 In mace ba ta da abin rufuwa, sai tă kasance mai aski kwal a kanta, amma da yake abin kunya ne mace tă yanke ko tă aske kanta, ya kamata tă sa yă yi girma kuma. 7 Bai kamata namiji yă kasance da dogon gashin kai ba

da kuka taru, ba Cimar Ubangiji kuke ci ba, [21] gama yayinda kuke ci, kowa yakan ci
gaba ba tare da jiran wani ba. Wani yǎ zauna da yunwa, wani kuma yǎ bugu. [22] Kai,
ba ku da gidajen da za ku ci ku sha ne? Ko dai kun rena ikkilisiyar Allah ne, kuna
kuma wulaƙanta waɗanda ba su da kome? Me zan ce muku? In yabe ku ne game
da wannan? A'a, ko kaɗan!

*Cimar Ubangiji*

[23] Gama abin da na karɓa daga wurin Ubangiji shi ne nake ba ku. Ubangiji Yesu, a
daren da aka bashe shi, ya ɗauki burodi, [24] bayan ya yi godiya, sai ya kakkarya ya ce,
"Wannan jikina ne, wanda yake dominku, ku yi wannan don tunawa da ni." [25] Haka
kuma bayan cimar, ya ɗauki kwaf, yana cewa, "Wannan kwaf ne sabon alkawari a
jinina; ku yi wannan, a duk sa'ad da kuke sha, don tunawa da ni." [26] Gama a duk
sa'ad da kuke cin wannan burodi, kuke kuma sha daga wannan kwaf, kuna shelar
mutuwar Ubangiji ne har yǎ dawo.

[27] Saboda haka, duk wanda ya ci burodin ko ya sha daga kwaf na Ubangiji da
rashin cancanta, ya yi laifin wulaƙanta jiki da jinin Ubangiji ke nan. [28] Dole kowa yǎ
bincike kansa kafin yǎ ci burodin yǎ kuma sha daga kwaf ɗin. [29] Gama duk wanda
ya ci ya kuma sha ba tare da fahimtar jikin Ubangiji ba, ya ci ya kuma sha wa kansa
hukunci ne. [30] Shi ya sa da yawa a cikinku ba su da ƙarfi, suna kuma da rashin lafiya,
waɗansunku kuma sun riga sun yi barci. [31] Amma in da za mu auna kanmu sosai, da
ba za mu shiga irin hukuncin nan ba. [32] Duk da haka sa'ad da Ubangiji ya hukunta
mu, ana yin mana horo ne don kada a ƙarshe a hallaka mu tare da duniya.

[33] Saboda haka 'yan'uwana, sa'ad da kuka taru don ci, ku jira juna. [34] In wani yana
jin yunwa, sai yǎ ci abinci a gida, saboda in kuka taru kada yǎ jawo hukunci.

Sa'ad da na zo kuma zan ba da ƙarin umarnai.

## 12

*Baye-bayen ruhaniya*

[1] To, game da baye-baye na ruhaniya, 'yan'uwa, ba na so ku kasance da rashin sani.
[2] Kun san cewa sa'ad da kuke masu bautar gumaka, ya zama, an shawo kanku, aka
kuma ɓad da ku ga bin gumaka marasa magana. [3] Saboda haka, ina gaya muku cewa
ba wani mai magana da ikon Ruhun Allah da zai ce, "Yesu la'ananne ne," haka kuma
ba wanda zai ce, "Yesu Ubangiji ne," sai wanda Ruhu Mai Tsarki yake bi da shi.

[4] Akwai baye-baye iri dabam-dabam, amma Ruhu ɗaya ne. [5] Akwai hidimomi iri-
iri, amma Ubangiji ɗaya ne. [6] Akwai aiki iri-iri, amma duk Allah ɗaya ne yake aikata
su a cikin dukan mutane.

[7] An ba wa kowane mutum bayyanuwar Ruhu don amfanin kowa. [8] Ga wani, an ba
shi saƙon hikima ta wurin Ruhu, ga wani baiwar saƙon sani ta wurin wannan Ruhu
guda. [9] Ga wani bangaskiya ta wurin wannan Ruhu, ga wani kuma baiwar warkarwa
ta wurin wannan Ruhu guda. [10] Ga wani yin ayyukan banmamaki, ga wani annabci,
ga wani baiwar rarrabe ruhohi, ga wani baiwar magana da harsuna dabam-dabam,
ga wani har wa yau iya fassarar harsuna. [11] Duk waɗannan aiki ne na wannan Ruhu
guda, yana kuma ba da su ga kowane mutum, yadda yake so.

[12] Jiki guda ne, ko da yake an yi shi da gaɓoɓi da yawa; gaɓoɓin kuma ko da yake
da yawa suke, jiki ɗaya ne. Haka yake da Kiristi. [13] Dukanmu an yi mana baftisma ta
wurin Ruhu guda zuwa ga jiki guda, ko Yahudawa ko Hellenawa, bawa ko 'yantacce,
an kuma ba wa dukanmu wannan Ruhu guda mu sha. [14] To, ba a yi jiki da gaɓa ɗaya
kawai ba, amma da gaɓoɓi da yawa.

[15] Da ƙafa za tǎ ce, "Saboda ni ba hannu ba ce, ni ba gaɓar jiki ba ce." Wannan
ba zai hana ta zama gaɓar jikin ba. [16] Da kunne zai ce, "Saboda ni ba ido ba ne, ni

ba gaɓar jiki ba ne.” Wannan ba zai hana shi zama gaɓar jikin ba. 17 Da a ce dukan
jiki ido ne, da me za a ji? Da kuma a ce dukan jiki kunne ne, da me za a sansana?
18 Tabbatacce, Allah ya shirya gaɓoɓin jiki, kowannensu, kamar yadda yake so su
zama. 19 Da a ce dukan jiki gaɓa ɗaya ne, da ina sauran jikin? 20 Yadda yake dai,
akwai gaɓoɓi da yawa, amma jiki ɗaya.

21 Ba dama ido ya ce wa hannu, “Ba na bukatarka ba!” Kai kuma ba zai ce wa
ƙafafu, “Ba na bukatarku ba!” 22 A maimakon haka, gaɓoɓin jiki da ake gani kamar
ba su da ƙarfi, su ne masu muhimmanci. 23 Kuma gaɓoɓin da muke tsammani ba
su da martaba sosai, su ne mukan fi ba su girma. Sa'an nan gaɓoɓi marasa kyan
gani, mun fi mai da hankali a kansu, 24 gaɓoɓi masu kyan gani kuwa, ba su bukatar
yawan girmamawa. Allah ya harhaɗa jikunanmu yadda gaɓoɓin da ake gani kamar
ba su da muhimmanci suna da amfani, 25 don kada rarrabuwa ta kasance a jiki, sai
dai gaɓoɓin jiki su kula da juna. 26 In wata gaɓa tana a damuwa, duk sai su damu
tare. In kuma an ɗaukaka wata gaɓa, sai duk su yi farin ciki tare.

27 To, ku jikin Kiristi ne, kowannenku kuwa gaɓarsa ne. 28 A cikin ikkilisiya, da farko
dai Allah ya zaɓa waɗansu ya naɗa su su zama manzanni, na biyu annabawa, na
uku malamai, sa'an nan masu yin ayyukan banmamaki, sai masu baiwar warkarwa,
da masu taimakon waɗansu, da masu baiwar gudanarwa, sa'an nan kuma masu
magana da harsuna iri-iri. 29 Shin, duka ne manzanni? Duka ne annabawa? Duka
ne malamai? Duka ne suke da baiwar yin ayyukan banmamaki? 30 Duka ne suke da
baiwar warkarwa? Duka ne suke magana da harsuna? Duka ne suke iya fassara?
31 Sai dai ku yi marmarin neman baye-baye mafi girma.

Yanzu kuwa zan nuna muku mafificiyar hanya.

# 13

*Kauna*

1 In ina iya yin magana da harsunan* mutane, da na mala'iku, amma ba ni da
ƙauna, na zama kamar kuge mai yawan ƙara, ko kuma ƙararrawa mai amo kawai.
2 In ina da baiwar annabci, ina kuma iya fahimtar dukan asirai da dukan ilimi, in
kuma ina da bangaskiyar da zan iya kawar da manyan duwatsu, amma ba ni da
ƙauna, ni ba kome ba ne. 3 In na ba wa matalauta dukan abin da nake da shi, na
kuma miƙa jikina a ƙone, amma ba ni da ƙauna, ban yi riban kome ba.

4 Kauna tana da haƙuri, ƙauna tana da kirki. Ba ta kishi, ba ta burga, ba ta da
girman kai. 5 Ba ta rashin ladabi, ba ta sonkai, ba ta da saurin fushi, ba ta riƙe
mutum a zuciya. 6 Kauna ba ta jin daɗin mugunta, sai dai ta ji daɗin gaskiya. 7 Tana
kāriya kullum, tana amincewa kullum, tana bege kullum, tana jimrewa kullum.

8 Kauna ba ta ƙarewa. Amma in akwai annabci zai shuɗe, harsuna su ɓace, ilimi
kuma zai ƙare. 9 Gama saninmu ba cikakke ba ne, annabcinmu kuma ba cikakke ba
ne. 10 Sai dai sa'ad da cikakken ya zo, sai wanda ba cikakke yǎ shuɗe. 11 Sa'ad da
nake yaro, na yi magana kamar yaro, na yi tunani kamar yaro, na yanke shawara
kamar yaro. Da na isa mutum kuwa, sai na bar halin yarantakata. 12 Yanzu kam
muna ganin abubuwa kamar a madubi sai dai ba sosai ba, amma a ranan nan za mu
gani fuska da fuska. Yanzu kam sanina ba cikakke ba ne, amma a ranan nan zan
kasance da cikakken sani, kamar dai yadda Allah ya san ni a yanzu.

13 Yanzu kam abubuwan nan uku sun tabbata, bangaskiya, bege, da kuma ƙauna.
Sai dai mafi girma a cikinsu ita ce ƙauna.

* **13:1** Ko kuwa yarurruka

# 14

*Baye-bayen annabci da kuma na harsuna*

1 Ku bi halin ƙauna kuna kuma marmarin neman baye-bayen ruhaniya, musam-
man baiwar annabci. 2 Gama duk wanda yake magana da wani harshe* ba da mutane
yake magana ba, sai dai da Allah. Tabbatacce, ba wanda yake fahimtarsa; yana faɗin
asirai ta wurin ruhu ne. 3 Amma duk wanda yake annabci, yana magana ne da
mutane domin yă gina su, yă ƙarfafa su, yă kuma yi musu ta'aziyya. 4 Wanda yake
magana da wani harshe kuwa, kansa yake gina, amma mai annabci, ikkilisiya ce yake
gina. 5 Zan so kowannenku yă yi magana da harsuna, sai dai zan fi so ku yi annabci.
Wanda yake annabci ya fi wanda yake magana da harsuna, sai dai in ya fassara don
ikkilisiya ta ginu.

6 To, 'yan'uwa, a ce na zo wurinku ina kuma yin magana da waɗansu harsuna,
amfanin me zan yi muku in ban zo muku da wani bayani ko sani ko annabci, ko
kuma kalmar koyarwa ba? 7 Abubuwan nan marasa rai ma da sukan yi ƙara, kamar
su algaita ko molo, in muryarsu ba tă fita sosai ba, yaya wani zai san abin da ake
busawa ko kaɗawa? 8 Haka ma in ba a busa ƙaho sosai ba, wa zai yi shirin yaƙi?
9 Haka yake sa'ad da kuka yi magana da waɗansu harsunan da ba a fahimta. In babu
wanda zai san abin da kuke faɗi, za ka dai yi wa iska magana ne kawai. 10 Ba shakka
akwai harsuna iri-iri a duniya, duk da haka kowane a cikinsu yana da ma'ana. 11 To,
in ban gane ma'anar abin da wani yake faɗi ba, ni baƙo ne ga mai maganar, shi
kuma baƙo ne a gare ni. 12 Haka yake a gare ku. Da yake kuna marmarin samun
baye-bayen ruhaniya, sai ku ba da ƙarfinku ga yin amfani da waɗanda za su gina
ikkilisiya.

13 Saboda haka, duk wanda yake magana da harshe, sai yă yi addu'a a yi masa
baiwar fassara. 14 Gama in na yi addu'a da wani harshe, ruhuna ne yake addu'a,
amma tunanina bai amfana kome ba. 15 To, me zan yi? Akwai lokutan da zan yi
addu'a da ruhuna; akwai kuma lokutan da zan yi addu'a da hankalina. Wani lokaci
ya kamata in yi waƙa da ruhuna, a wani lokacin kuma in yi waƙa da hankalina. 16 A
cewa waɗansu baƙi suna cikin sujadarku, sa'ad da kuke yabon Allah da ruhunku,
yaya waɗanda suke tare ku za su fahimta, har su ce, "Amin," da yake ba su san abin
da kuke faɗi ba? 17 Ko da yake kuna ba da godiya da kyau, amma wancan mutumin
da yake tare da ku bai ginu ba.

18 Na gode wa Allah, domin ina magana da harsuna fiye da ku duka. 19 Amma a
cikin ikkilisiya zan gwammace in yi magana da kalmomi biyar da za a fahimta don in
koyar da waɗansu da a ce in yi magana da kalmomi guda dubu goma a wani harshe.

20 'Yan'uwa, ku daina tunani kamar yara. Wajen mugunta ku zama jarirai, sai dai
wajen tunaninku, ku zama manya. 21 A cikin Doka yana a rubuce cewa,

"Ta wurin mutane masu baƙin harsuna
   da kuma ta leɓunan baƙi
zan yi magana da waɗannan mutane,
   amma duk da haka, ba za su saurare ni ba,"†
   in ji Ubangiji.

22 Harsuna fa alama ce ba ga masu bi ba, sai dai ga marasa bi. Annabci kuwa ga
masu bi ne ba ga marasa bi ba. 23 Saboda haka, in dukan ikkilisiya ta taru, kowa
kuma yana magana da waɗansu harsuna, sai waɗansu jahilai ko waɗansu marasa bi
suka shigo, ashe, ba za su ce kuna hauka ba? 24 Amma in wani marar bi, ko jahili ya
shigo sa'ad da kowa yana annabci, sai maganar kowa ta ratsa shi, za su shawo kansa
yă gane cewa shi mai zunubi ne saboda abin da kowa yake faɗi, 25 asirin zuciyarsa

* **14:2** Ko kuwa wani yare; haka ma a ayoyi 4, 13, 14, 19, 26 da 27 † **14:21** Ish 28.11,12

kuma su bayyana a fili. Don haka, zai fāɗi a ƙasa yă yi wa Allah sujada yana cewa, “Lalle, Allah yana cikinku!”

### *Tsarin sujada*

26 Me za mu ce ke nan ’yan’uwa? Sa’ad da kuka taru, wani yakan yi waƙa, wani
koyarwa, wani wahayi, wani yin magana da wani harshe, wani kuma fassara. Dole
ne a yi duka don gina ikkilisiya. 27 In kuwa waɗansu za su yi magana a wani harshe,
to, kada su fi mutum biyu ko uku, kuma a yi bi da bi, wani kuma yă fassara. 28 In babu
mai fassara, sai mai magana yă yi shiru a cikin ikkilisiya, yă yi wa kansa magana da kuma Allah.
29 Annabawa biyu ko uku za su iya yin magana, sauran kuma sai su auna a hankali
abin da aka faɗa. 30 In kuma wahayi ya zo wa wani da yake zaune, sai mai magana
na farko yă yi shiru. 31 Dukanku kuna iya yin annabci bi da bi, domin kowa yă
sami koyarwa da ƙarfafawa. 32 Ruhohin annabawa kuwa suna ƙarƙashin sarrafawar
annabawa. 33 Gama Allah, ba Allah mai sa rikicewa ba ne, sai dai mai salama. Kamar yadda yake a dukan ikkilisiyoyi na tsarkaka.
34 Ya kamata mata su zauna shiru a cikin ikkilisiyoyi. Ba su da izinin yin magana,
sai dai su yi biyayya yadda Doka ta faɗi. 35 In suna so su yi tambaya game da wani
abu, ya kamata su tambayi mazansu a gida, domin abin kunya ne mace tă yi magana a cikin ikkilisiya.
36 Shin, a kanku ne maganar Allah ta fara? Ko kuma a gare ku ne kaɗai ta iso? 37 In
wani yana tsammani shi annabi ne, ko yana da baiwar ruhaniya, bari yă gane cewa
abin da nake rubuta muku umarnin Ubangiji ne. 38 In ya ƙi kula da wannan, shi ma sai a ƙi kula da shi.
39 Saboda haka ’yan’uwana, ku yi marmarin yin annabci, kada kuma ku hana
magana da harsuna. 40 Sai dai a yi kome daidai da kuma cikin tsari.

## 15

### *Tashin matattu na Kiristi*

1 To, ’yan’uwa, ina so in tuna muku da bisharar da na yi muku wa’azinta, wadda
kuka karɓa, wadda kuma kuka yanke shawara ku tsaya a kai. 2 Ta wurin wannan
bisharar ce kuka sami ceto, muddin kuna riƙe da wa’azin da na yi muku kam-kam. In ba haka ba, kun gaskata a banza ke nan.
3 Gama abu farko mafi muhimmancin da na karɓo shi ne na ba ku cewa Kiristi ya
mutu domin zunubanmu bisa ga Nassi, 4 cewa an binne shi an kuma tashe shi a rana
ta uku bisa ga Nassi, 5 cewa ya bayyana ga Bitrus, sa’an nan ga Sha Biyun. 6 Bayan
haka, ya bayyana ga fiye da ɗari biyar daga cikin ’yan’uwa a lokaci guda. Yawancinsu
kuwa suna nan da rai, ko da yake waɗansu sun riga sun yi barci. 7 Sa’an nan ya
bayyana ga Yaƙub, sa’an nan ga dukan manzannin, 8 a ƙarshe duka, ya bayyana a gare ni, kamar wanda an haifa a lokacin da bai kamata ba.
9 Gama ni ne mafi ƙanƙanta a cikin manzanni, ban kuma isa a kira ni manzo ba,
domin na tsananta wa ikkilisiyar Allah. 10 Amma bisa ga alherin Allah, na zama abin
da nake, alherinsa zuwa gare ni kuwa bai zama a banza ba. A’a, na yi aiki fiye da
dukansu, duk da haka, ba ni ba ne, sai dai alherin Allah da yake tare da ni ne. 11 To,
ko ni ne, ko su ne, wannan shi ne abin da muke wa’azi, shi ne kuma abin da kuka gaskata.

### *Tashin matattu na waɗanda suka mutu*

12 Amma in ana wa’azi cewa Kiristi ya tashi daga matattu, yaya waɗansu a cikinku
suke cewa babu tashin matattu? 13 In babu tashin matattu, to, ba a tā da Kiristi ma ba
ke nan. 14 In ba a tashe Kiristi ba kuwa, ai, wa’azinmu, da bangaskiyarku banza ne.

15 Sai ma ya zama mun zama masu ba da shaidar ƙarya game da Allah ke nan, domin
mun shaida game da Allah cewa ya tashe Kiristi daga matattu. Bai tashe Kiristi ba ke
nan, in lalle ba a tā da matattu. 16 Gama in ba a tā da matattu ba, to, Kiristi ma ba
a tashe shi ba ke nan. 17 In kuwa ba a tashe Kiristi ba, bangaskiyarku a banza take,
ya zama har yanzu kuna cikin zunubanku ke nan. 18 Ashe, waɗanda suka yi barci a
cikin Kiristi ma sun hallaka ke nan. 19 In a wannan rayuwar ce kaɗai muke da bege
cikin Kiristi, mun zama abin tausayi fiye da dukan mutane.
20 Amma tabbatacce, an tā da Kiristi daga matattu, nunan fari kuwa cikin waɗanda
suka yi barci. 21 Da yake mutuwa ta zo ta wurin mutum, haka tashin matattu ma ya
zo ta wurin mutum. 22 Kamar yadda duka suka mutu cikin Adamu, haka duka za
su rayu cikin Kiristi. 23 Sai dai kowa da lokacinsa. Kiristi ne nunan fari; sa'an nan
sa'ad da ya dawo; za a tā da waɗanda suke nasa. 24 Sa'an nan sai ƙarshen ta zo,
sa'ad da zai miƙa wa Allah Uba mulki, bayan ya hallaka dukan sarauta, mulki da iko.
25 Gama dole yǎ yi mulki har sai ya sa dukan abokan gābansa a ƙarƙashin ƙafafunsa.
26 Abokin gāba na ƙarshen da za a hallaka kuwa, shi ne mutuwa. 27 Gama ya "sa
kome a ƙarƙashin ƙafafunsa."* To, da aka ce an sa "kome" a ƙarƙashinsa, a fili yake
cewa ba a haɗa da Allah a ciki ba, shi wannan da ya sa kome a ƙarƙashin Kiristi.
28 Sa'ad da ya yi haka, sa'an nan Ɗan kansa yǎ koma a ƙarƙashin shi wanda ya sa
kome a ƙarƙashinsa, domin Allah yǎ zama kome da kome.
29 To, in babu tashin matattu, mene ne waɗanda ake musu baftisma saboda matattu
za su yi? In ba a tā da matattu sam, me ya sa ake yin wa mutane baftisma saboda
su? 30 Mu ma don me muke sa kanmu cikin hatsari a kowace sa'a? 31 Ina fuskantar
mutuwa kowace rana. I, kamar yadda yake tabbatacce cewa ina taƙama da ku cikin
Kiristi Yesu Ubangijinmu. 32 In na yi kokawa da mugayen namomin jeji a Afisa bisa
ga ra'ayin mutane ne kawai, mece ce ribata, in har ba a tā da matattu? Ai,
"Sai mu ci mu sha,
da yake gobe za mu mutu."†
33 Kada fa a ruɗe ku, "Ajiyar mugayen abokai yana ɓata hali mai kyau." 34 Ku koma
cikin hankalinku yadda ya kamata, ku kuma daina yin zunubi, gama akwai waɗansu
da ba su san Allah ba, na faɗi wannan ne don ku kunyata.

*Tashin jiki*

35 Amma wani yana iya tambaya yǎ ce, "Ta yaya ake tā da matattun? Da wane irin
jiki za su tashi?" 36 Kai, marar azanci! Abin da kuka shuka ba zai tsira ba sai ya mutu.
37 Sa'ad da kuke shuki, ba tsiron da zai yi girma ba ne kuka shuka, ƙwayar ce kawai,
ko ta alkama ko kuma na wani irin dabam. 38 Amma Allah yakan ba ƙwayar jiki
yadda ya yi niyya, kuma ga kowane irin ƙwaya yakan ba ta irin jikinta. 39 Ba dukan
nama ne iri ɗaya ba. Mutane da irin nasu, dabbobi da irin nasu, tsuntsaye da irin
nasu, kifaye kuma da irin nasu. 40 Akwai jikuna iri na samaniya, akwai kuma jikuna
iri na duniya; sai dai darajar jikunan samaniya dabam take, darajar jikunan duniya
kuma dabam take. 41 Rana tana da wata irin daraja, wata yana da wata darajar
dabam, taurari kuma suna da tasu dabam. Wani tauraro kuwa yakan bambanta da
wani a wajen daraja.
42 Haka ne tashin matattu zai kasance. Abin da aka shuka yakan ruɓe, abin da aka
tā da shi kuma ba ya ruɓewa; 43 akan shuka shi cikin ƙasƙanci, a kuma tā da shi
cikin ɗaukaka, akan shuka shi da rashin ƙarfi, a kuma tā da shi da ƙarfi; 44 akan
shuka shi da jiki na mutuntaka, a kuma tā da shi da jikin ruhaniya.
In akwai jiki na mutuntaka, to, lalle akwai jikin ruhaniya ma. 45 Haka yake a
rubuce cewa, "Adamu, mutumin farko ya zama mai rai"‡; Adamu na ƙarshe kuwa

* **15:27** Zab 8.6 † **15:32** Ish 22.13 ‡ **15:45** Far 2.7

ruhu ne mai ba da rai. 46 Ba jikin ruhaniya ne ya zo da farko ba, na mutuntakan ne,
daga baya kuma sai na ruhaniya. 47 Mutumin farko daga turɓaya ce ya fito, mutum
na biyu kuwa daga sama ne ya fito. 48 Kamar yadda mutumin turɓaya yake, haka
ma waɗanda suke na turɓaya. Kuma kamar yadda mutumin sama yake, haka ma
waɗanda suke na sama. 49 Kamar dai yadda muka ɗauki siffar mutumin turɓaya,
haka kuma za mu ɗauki siffar mutumin sama.
50 Ina sanar da ku, ʼyanʼuwa, cewa nama da jini ba za su gāji mulkin Allah ba,
haka ma ruɓa ba zai gāji rashin ruɓa ba. 51 Ku saurara, in gaya muku wani asiri. Ba
dukanmu ne za mu yi barci ba, sai dai duk za a sauya kamanninmu 52 farat ɗaya, cikin
ƙyaftawar ido, da busan ƙaho na ƙarshe. Gama za a busa ƙaho, za a tā da matattu
da jiki irin da ba ya ruɓewa, za a kuma sauya kamanninmu. 53 Gama dole mai ruɓa
yă maye wa mai ruɓan nan, marar mutuwa kuma yă maye wa mai mutuwan nan.
54 Saʼad da mai ruɓan nan ya maye marar ruɓan nan, mai mutuwa kuma ya maye
marar mutuwan nan, saʼan nan ne karin maganar da yake a rubuce zai zama gaskiya
cewa, "An haɗiye mutuwa cikin nasara."§
55 "Ya ke mutuwa, ina nasararki?
Ya ke mutuwa, ina dafinki?"*
56 Zunubi ne yake ba wa mutuwa dafi, Doka kuma take ba wa zunubi iko. 57 Amma
godiya ga Allah! Shi ne ya ba mu nasara ta wurin Ubangijinmu Yesu Kiristi.
58 Saboda haka, ƙaunatattu ʼyanʼuwana, ku tsaya da daram. Kada wani abu yă
jijjiga ku. Ku ba da kanku kullum ga aikin Ubangiji, domin kun san cewa famar da
kuke yi saboda Ubangiji ba a banza take ba.

# 16

*Bayarwa saboda mutanen Allah*

1 To, game da tara kuɗi domin taimakon mutanen Allah, ku yi abin da na gaya wa
ikkilisiyoyin Galatiyawa. 2 A ranar farko ta kowace mako, ya kamata kowannenku yă
keɓe ʼyan kuɗi bisa ga abin da yake samu, yă ajiye, ba sai na zo kafin a tara taimakon
ba. 3 In kuwa na iso sai in ba da wasiƙun gabatarwa ga mutanen da kuka amince da
su, in kuma aike su da taimakonku zuwa Urushalima. 4 In kuma ya dace in tafi, to,
sai su tafi tare da ni.

*Roƙona*

5 Bayan na zazzaga Makidoniya, zan zo wurinku, domin zan ratsa ta Makidoniya.
6 Wataƙila zan ɗan jima a wajenku, ko ma in ci damina a can, domin ku yi mini
rakiya a tafiyata, duk inda za ni. 7 Ba na so in gan ku yanzu in wuce kawai, ina fata
zan yi ʼyan kwanaki tare da ku, in Ubangiji ya yarda. 8 Sai dai zan kasance a Afisa har
lokacin Fentekos, 9 domin an buɗe mini wata hanya mai fāɗi don aiki mai amfani,
ko da yake akwai mutane da yawa masu gāba da ni.
10 In Timoti ya zo, ku tabbata ya sami sakewa a cikinku, domin aikin Ubangiji yake
yi kamar yadda nake yi. 11 Kada fa wani yă ƙi karɓansa. Ku sallame shi lafiya, domin
yă koma wurina. Ina duban hanyarsa tare da ʼyanʼuwa.
12 Batun ɗanʼuwanmu Afollos kuwa, na roƙe shi sosai yă zo wurinku tare da
ʼyanʼuwa. Bai so zuwa yanzu ba, amma zai zo in ya sami zarafi.
13 Ku zauna a faɗake; ku dāge cikin bangaskiya; ku zauna da ƙarfafawa; ku yi
ƙarfi. 14 Ku yi kome da ƙauna.
15 Kun san cewa iyalin gidan Istifanas ne suka fara tuba a Akayya. Sun kuma ba
da kansu ga yi wa tsarkaka hidima. Ina roƙonku ʼyanʼuwa, 16 ku ba da kanku ga irin
waɗannan, ga kuma kowa da ya haɗa hannu a aikin, yana kuma faman a cikinsa.

§ **15:54** Ish 25.8 * **15:55** Hos 13.14

17 Na yi farin ciki da isowar Istifanas, Fortunatus da Akaikus, domin sun biya bukatar
da ba ku iya biya ba. 18 Gama sun wartsake ruhuna da kuma naku. Ya kamata ku
girmama irin waɗannan mutane.

### *Gaisuwa ta ƙarshe*

19 Ikkilisiyoyin da suke a lardin Asiya suna gaisuwa.

Akwila da Firiskila suna gaishe ku sosai cikin Ubangiji, haka ma ikkilisiyar da takan taru a gidansu.

20 Dukan 'yan'uwa a nan suna gaisuwa.

Ku gai da juna da sumba mai tsarki.

21 Ni, Bulus nake rubuta wannan gaisuwa da hannuna.

22 Duk wanda ba ya ƙaunar Ubangiji, la'ana ta zauna a kansa. Zo, ya Ubangiji*!

23 Alherin Ubangiji Yesu yă kasance tare da ku.

24 Ina gaishe ku duka, gaisuwar ƙaunata cikin Kiristi Yesu. Amin.†

* **16:22** Da Arameyik kalman nan Zo, ya Ubangiji ita ce Maranata. † **16:24** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā ba su da Amin.

# 2 Korintiyawa

1 Bulus, manzon Kiristi Yesu ta wurin nufin Allah, da kuma daga Timoti
ɗan'uwanmu,

Zuwa ga ikkilisiyar Allah da take a Korint, tare da dukan tsarkaka a ko'ina a Akayya.

2 Alheri da salama daga Allah Ubanmu da kuma Ubangiji Yesu Kiristi, su kasance
tare da ku.

### *Allah na dukan ta'aziyya*

3 Yabo ya tabbata ga Allah, da Uban Ubangijinmu Yesu Kiristi, Uba mai tausayi,
da kuma Allah na dukan ta'aziyya, 4 wanda yakan yi mana ta'aziyya a cikin dukan
wahalolinmu, domin mu kuma mu iya ta'azantar da waɗanda suke cikin kowace irin
wahala, da ta'aziyyar da mu kanmu muka samu daga Allah. 5 Gama kamar yadda
wahalar Kiristi ta cika har tana zuba a cikin rayuwarmu, haka nan kuma ta wurin
Kiristi ta'aziyyarmu ta cika har tana zuba. 6 In muna shan wahala, ai, muna shanta
domin ta'aziyyarku, da cetonku ne, in mun sami ta'aziyya, ai, mun same ta domin
ta'aziyyarku ce, wadda take sa ku jure wa irin wahalan nan, da muke sha. 7 Begen
da muke da shi dominku kuwa, tabbatacce ne, domin mun san cewa kamar yadda
kuke tarayya da mu a cikin wahalolinmu, haka kuma kuke tarayya da mu a cikin
ta'aziyyarmu.
8 'Yan'uwa, ba ma so ku zama da rashin sani, a kan wahalolin da muka sha a
lardin Asiya. Mun sha wahaloli sosai, har abin ya fi ƙarfinmu, ya sa muka fid da
tsammanin rayuwa. 9 Ba shakka, a zuciyarmu mun ji kamar hukuncin kisa ne aka yi
mana. Wannan kuwa ya faru ne domin kada mu dogara da kanmu, sai dai ga Allah,
wanda yake tā da matattu. 10 Shi ya cece mu daga irin wannan hatsari na mutuwa,
zai kuwa cece mu. A kansa muka kafa bege cewa zai ci gaba da cetonmu, 11 yayinda
kuke taimakonmu ta wurin addu'o'inku. Mutane da yawa kuwa za su yi godiya ta
dalilinmu, saboda albarkar da aka yi mana, ta amsa addu'o'i masu yawa.

### *Canja shirye-shiryen Bulus*

12 Wannan shi ne taƙamarmu. Lamirinmu yana ba da shaida cewa mun yi
zamanmu a duniya, musamman a dangantakarmu da ku cikin tsarki, tsakani da
Allah. Mun yi haka ta wurin bishewar alherin Allah, ba bisa ga hikimar duniya
ba. 13 Gama ba mu rubuta muku abin da ba za ku iya karatu ko ku kāsa fahimta ba.
Ina kuma fata cewa, 14 kamar yadda kuka ɗan fahimce mu, za ku kai ga cikakkiyar
fahimta cewa za ku iya yin taƙama da mu, kamar yadda mu ma za mu yi taƙama da
ku a ranar da Ubangiji Yesu zai dawo.
15 Saboda na amince da haka, shi ya sa na so zuwa wurinku da fari, domin ku
sami albarka riɓi biyu. 16 Na yi shiri in ziyarce ku a kan hanyata zuwa Makidoniya,
in kuma sāke dawo wurinku a kan hanyata daga Makidoniya, sa'an nan ku yi mini
rakiya a hanyata zuwa Yahudiya. 17 Kuna gani na yi wannan shirin ba da sanin abin
da nake yi ba ne? Ko kuwa, kuna gani na yi shirin nan da halin mutuntaka ne, don
in ce, "I" in koma in ce, "A'a"?
18 Kamar dai yadda ba shakka Allah yake mai aminci, haka ma maganar da muka yi
muku, ba "I" da kuma "A'a" ba ce. 19 Gama Ɗan Allah, Yesu Kiristi, wanda ni da Sila
da Timoti muka yi muku wa'azinsa, ai, ba "I" da "A'a" ba ne, amma a cikin Kiristi,
"I" ne kullum. 20 Domin dukan alkawaran Allah cikarsu a gare shi suke, ta wurinsa

ne kuma muke faɗar “Amin”, domin a ɗaukaka Allah. 21 Allah ne fa yake sa mu da
ku mu tsaya daram cikin Kiristi. Shi ne ya shafe mu, 22 ya buga mana hatiminsa a
kan mu nasa ne, ya kuma sa mana Ruhunsa a cikin zukatanmu, domin yă tabbatar
da abin da yake zuwa nan gaba.
23 Labudda, Allah shi ne shaidata cewa don kada in ƙara muku wahala ne ya sa ban
koma Korint ba. 24 Ba nuna muku iko a kan bangaskiyarku muke yi ba, sai dai muna
aiki tare da ku ne saboda farin cikinku, domin bisa ga bangaskiya ce kuke tsaye da
ƙarfi.

# 2

1 Saboda haka na yanke shawara ba zan sāke kawo muku ziyara ta ɓacin rai ba.
2 Gama in na sa ku baƙin ciki, wa ya rage yă faranta mini zuciya, in ba ku waɗanda na
sa baƙin cikin ba? 3 Na rubuta yadda na yi ne saboda sa’ad da na iso kada waɗanda
ya kamata su faranta mini rai, su sa ni baƙin ciki. Na amince da ku duka a kan farin
cikina naku ne ku duka. 4 Gama na rubuta muku ne cikin baƙin ciki mai yawa da
ɓacin zuciya har ma da hawaye mai yawa, ba don in sa ku baƙin ciki ba ne, a’a, sai
dai domin in nuna muku zurfin ƙaunar da nake yi muku.

### *Gafara don mai zunubi*

5 In wani ya jawo baƙin ciki, ba ni kaɗai ya jawo wa ba, amma a wani fanni, sai
in ce dukanku ne ya jawo wa, ba na faɗa haka don in matsa muku lamba ba ne.
6 Irin wannan mutum, horon da yawancin mutane suka yi masa ya isa haka. 7 Yanzu
fa, a maimako, gara ku yafe masa, ku kuma ta’azantar da shi, don kada baƙin ciki
mai yawa yă sha kansa. 8 Saboda haka, ina roƙonku, ku sāke nuna masa ƙaunarku.
9 Abin da ya sa na rubuta muku shi ne don in ga ko za ku jimre da gwajin nan, kuna
kuma yin biyayya ta kowace hanya. 10 In kuka gafarta wa wani, ni ma na gafarta
masa. Abin da na gafarta kuwa, in har ma da abin gafartawa, saboda ku ne na gafarta
masa, albarkacin Kiristi, 11 don kada Shaiɗan yă rinjaye mu. Da yake muna sane da
dabarunsa.

### *Masu hidimar sabon alkawari*

12 To, sa’ad da na tafi Toruwas don in yi wa’azin bisharar Kiristi, ko da yake na
tarar cewa Ubangiji ya buɗe mini ƙofa, 13 duk da haka, ban sami salama a zuciyata
ba domin ban sami ɗan’uwana Titus a can ba. Sai na yi bankwana da su na wuce
zuwa Makidoniya.
14 Amma godiya ga Allah, wanda kullum yake bi da mu da nasara cikin Kiristi,
kuma ta wurinmu, yana baza ƙanshin nan na sanin Kiristi a ko’ina. 15 Don kuwa, a
wurin Allah mu ƙanshin Kiristi ne cikin waɗanda ake ceto, da kuma waɗanda suke
hanyar hallaka. 16 Ga wani, mu warin mutuwa ne, amma ga wani kuwa, mu ƙanshin
rai ne. Wa ya isa yă yi irin wannan aikin? 17 Ba ma tallar maganar Allah don riba
yadda waɗansu mutane da yawa suke yi. A maimakon haka, muna magana cikin
Kiristi a gaban Allah da gaskiya, kamar mutanen da aka aika daga Allah.

# 3

1 Yabon kanmu ne kuma muka fara yi? Ko kuwa muna bukatar wasiƙun yabo ne
zuwa gare ku, ko daga gare ku, kamar yadda waɗansu suke yi? 2 Ai, ku kanku ku ne
wasiƙarmu, wadda aka rubuta a zukatanku, domin kowa yă santa, yă kuma karanta
ta. 3 Kun nuna cewa ku wasiƙa ce daga Kiristi, sakamakon hidimarmu, ba wadda aka
rubuta da inki ba, sai dai da Ruhun Allah mai rai. Ba kuma a kan allunan dutse ba,
sai dai a kan allunan zukatan mutane.
4 Amincewa kamar wannan shi ne namu ta wurin Kiristi a gaban Allah. 5 Ba mu
da wani abin da za mu nuna cewa da iyawarmu ne muke aikin nan. Iyawarmu daga

wurin Allah ne. 6 Shi ya sa muka gwaninta a matsayinmu na masu hidimar sabon
alkawari ba ta rubutacciyar Dokar ba, amma ta Ruhu; don Dokar, kisa take yi, Ruhu
kuwa yana ba da rai.

*Daukakar sabon alkawari*

7 To, in hidimar da ta kawo mutuwa, wadda an rubuta a kan allon dutse, ta zo da
ɗaukaka har Isra'ilawa suka kāsa duban fuskar Musa saboda tsananin haskenta, ko
da yake mai shuɗewa ce, 8 ashe, hidimar Ruhu ba za tă fi wannan ɗaukaka ba? 9 In
hidimar da take jawo wa mutane hukunci tana da ɗaukaka haka, to, lalle, hidimar
da take kawo adalci za tă fi ta ɗaukaka nesa! 10 Gama abin da dā take da ɗaukaka,
ba ta da ɗaukaka a yanzu, in aka kwatantata da mafificiyar ɗaukaka ta yanzu. 11 In
kuma aba mai shuɗewa ta zo da ɗaukaka, ashe, abin da yake dawwammame, lalle
ne yă kasance da ɗaukakar da ta fi haka nesa!
12 Da yake muna da bege irin wannan, to, muna da ƙarfin zuciya sosai ke nan. 13 Mu
ba kamar Musa ba ne, wanda ya rufe fuskarsa da lulluɓi, don kada Isra'ilawa su ga
ƙarewar ɗaukakan nan mai shuɗewa. 14 Amma aka sa hankulansu suka dushe, gama
har yă zuwa yau akwai lulluɓin nan a duk sa'ad da ake karatun tsohon alkawari. Ba
a kawar da shi ba, sai a cikin Kiristi ne kaɗai ake kawar da shi. 15 Har yă zuwa
yau, duk sa'ad da ake karatun littattafan Musa, lulluɓin nan yakan rufe zukatansu.
16 Amma duk sa'ad da wani ya juyo ga Ubangiji, akan kawar da lulluɓin. 17 Ubangiji
fa, shi ne Ruhu, kuma duk inda Ruhun Ubangiji yake, a nan 'yanci yake. 18 Mu da ba
mu da lulluɓi a fuskokinmu duk muna nuna ɗaukakar Ubangiji, ana sauya mu mu
ɗauki kamanninsa cikin ɗaukaka mai hauhawa. Ubangiji wanda yake ruhu kuwa
shi ne mai zartar da haka.

# 4

*Dukiya cikin tulunan yumɓu*

1 Saboda haka, da yake ta wurin jinƙan Allah ne muke da wannan hidima, ba za
mu fid da zuciya ba. 2 Ba ruwanmu da ɓoye-ɓoye na munafuncin da suke abubuwan
kunya. Ba ruwanmu da ruɗu, ko yin ƙarya da kalmar Allah. Sai dai muna faɗin
gaskiya a fili. Ta haka ne kowa zai yi shaidar gaskiyarmu a gaban Allah cikin
zuciyarsa. 3 Ko da bisharármu a rufe take, tana a rufe ne ga waɗanda suke hallaka.
4 Allahn zamanin nan ya makanta hankulan marasa ba da gaskiya, yadda har ba za su
iya ganin hasken bishara ta ɗaukakar Kiristi ba, wanda yake kamannin Allah. 5 Gama
ba wa'azin kanmu muke yi ba, sai dai na Yesu Kiristi, a kan shi ne Ubangiji, mu kuma
bayinku saboda Yesu. 6 Domin shi Allah wanda ya ce, "Bari haske yă haskaka daga
duhu,"* ya sa haskensa ya haskaka a cikin zukatanmu, don yă ba mu hasken sanin
ɗaukakar Allah a fuskar Kiristi.
7 Amma muna da wannan dukiya a cikin tulunan yumɓu, don a nuna wannan
mafificin ikon nan daga Allah ne, ba daga gare mu ba. 8 A matse muke a kowane
gefe, sai dai ba a gurgunta mu ba. An rikitar da mu, amma ba mu fid da zuciya
ba. 9 An tsananta mana, amma ba a yashe mu ba, an fyaɗe mu da ƙasa, amma ba
a hallaka mu ba. 10 Kullum muna ɗauke da mutuwar Yesu a jikinmu, domin ran
Yesu yă bayyana a jikinmu. 11 Muddin muna a raye, kullum zaman mutuwa muke
yi saboda Yesu, don a bayyana ran Yesu ta wurin jikin nan namu mai mutuwa. 12 Ta
haka, mutuwa tana aiki a cikinmu, ku kuwa rai a cikinku.
13 A rubuce yake cewa, "Na gaskata; saboda haka na yi magana." Da wannan ruhun
bangaskiya ne mu ma muka gaskata, saboda haka muke magana. 14 Domin mun san
cewa shi da ya tā da Ubangiji Yesu daga matattu, zai tashe mu mu ma tare da Kiristi,
yă kuma miƙa mu a gabansa tare da ku. 15 Duk wannan fa don amfaninku ne, domin

* **4:6** Far 1.3

alherin nan da yake bazuwa zuwa ga mutane masu yawa, yǎ zama dalilin godiya mai
yawa ga ɗaukakar Allah.
16 Saboda haka, ba mu fid da zuciya ba. Ko da yake a waje, jikinmu mai mutuwa
yana lalacewa, amma can ciki, ana sabunta mu kowace rana. 17 Don wannan 'yar
wahalar tamu mai saurin wucewa, ita take tanadar mana madawwamiyar ɗaukaka
mai yawa, fiye da kwatanci. 18 Domin ba abubuwan da ido yake gani ne muke dubawa
ba, sai dai marasa ganuwa. Gama abubuwan da ake gani masu saurin wucewa ne,
marasa ganuwa kuwa, madawwama ne.

# 5

*Wurin zamanmu a sama*
1 Yanzu mun san cewa in an hallaka tentin duniyan nan da muke ciki, muna da
wani gini daga Allah, madawwamin gida a sama, wanda ba da hannuwan mutum ne
suka gina shi ba. 2 Kafin nan muna nishi, da marmari a yi mana sutura da gidanmu
na sama, 3 don sa'ad da aka yi mana sutura, ba za a same mu tsirara ba. 4 Sa'ad da
muke zaune a cikin jikin nan na duniya, nishi muke domin matsuwar da muke sha,
ba domin muna so mu rabu da jikinmu na wannan duniya ba ne, sai dai don so muke
yi a suturta mu da na Sama, domin mai rai ya shafe mai mutuwa. 5 Allah ne ya yi
mu domin wannan, ya kuma ba mu Ruhu a matsayin abin ajiya, yana kuma tabbatar
da abin da zai zo nan gaba.
6 Saboda haka, kullum muna da tabbaci mun kuma san cewa, muddin muna a
duniya cikin jikin nan, ana raba mu da Ubangiji. 7 Rayuwa bangaskiya muke, ba ta
ganin ido ba. 8 Ina cewa muna da tabbaci, za mu fi so mu rabu da jikin nan, mu kuma
kasance a sama tare da Ubangiji. 9 Saboda haka, niyyarmu ita ce, mu gamshe shi, ko
muna a duniya cikin jikin nan, ko ba mu nan. 10 Gama dole dukanmu mu bayyana
a gaban kujerar shari'ar Kiristi, domin kowannenmu yǎ karɓi ladan aikin da ya yi a
wannan jiki, ko mai kyau ne ko marar kyau.

*Hidimar sulhuntawa*
11 To, da yake mun san ko mene tsoron Ubangiji yake, muna ƙoƙari mu rinjaye
mutane. Yadda muke kuwa, yana sane a sarari ga Allah, ina kuma fata yana nan a
sarari a lamirinku. 12 Ba ƙoƙari muke mu yabe kanmu a gare ku ba ne, sai dai muna
ba ku damar yin taƙama da mu ne, don ku sami amsar da za ku ba wa waɗanda
suke taƙama da abin da ake gani ne, a maimakon abin da yake cikin zuciya. 13 In
hankalinmu a taɓe yake, ai, saboda Allah ne, in kuwa cikin hankalinmu muke, ai,
saboda ku ne. 14 Kaunar Kiristi a gare mu, ita take mallakarmu, saboda haka mun
tabbata, da yake wani ya mutu saboda dukan mutane, ashe kuwa, mutuwarsu ce
dukansu. 15 Ya kuwa mutu ne saboda dukan mutane, domin kada waɗanda suke
rayuwa kada su yi zaman ganin dama a nan gaba, sai dai su yi zaman wannan da ya
mutu saboda su, aka kuma tashe shi saboda su.
16 Saboda haka, daga yanzu zuwa nan gaba, ba mu ƙara ɗaukan wani mutum bisa
ga ganin duniya ba. Ko da yake a dā, mun ɗauki Kiristi haka, amma yanzu mun
daina yin haka. 17 Saboda haka, duk wanda yake cikin Kiristi, sabuwar halitta ce,
tsohon al'amari ya shuɗe, sabon ya zo! 18 Duk wannan kuwa daga Allah ne, wanda
ya sulhunta mu da kansa ta wurin Kiristi, ya kuma ba mu hidimar sulhu, 19 wato,
Allah ya sulhunta duniya zuwa kansa ta wurin Kiristi, ba ya lissafta zunuban mutane
a kansu. Ya kuma danƙa mana saƙon sulhu. 20 Saboda haka, mu jakadu ne na Kiristi,
sai ka ce Allah kansa yake magana ta wurinmu. Muna roƙonku a madadin Kiristi.
Ku sulhuntu da Allah. 21 Shi da bai san zunubi ba, Allah ya mai da shi kamar hadayar
zunubi saboda mu, domin mu sami adalcin Allah ta wurinsa.

# 6

1 A matsayinmu na abokan aikin Allah, muna roƙonku kada ku karɓi alherin Allah
a banza. 2 Gama ya ce,
"A lokacin samun alherina, na ji ka,
a ranar samun ceto kuma, na taimake ka."*
Ina gaya muku, yanzu ne lokacin samun alherin Allah, yanzu ne ranar samun ceto.

*Wahalolin Bulus*

3 Ba ma sa abin tuntuɓe wa kowa, domin kada hidimarmu ta zama abin zargi. 4 A
maimakon haka, duk abin da muke yi, muna yin shi ne don mu nuna cewa mu masu
hidimar Allah ne. Muna yin haka cikin jimrewa, da shan wahala, da shan wuya, har
da shan masifu. 5 Da shan dūka, da shan dauri, da yawan hargitsi, da yawan fama,
da rashin barci, da kuma yunwa. 6 Da cikin tsarki, da fahimta, da haƙuri, da kirki, da
cikin Ruhu Mai Tsarki, da cikin ƙauna mai gaskiya, 7 da cikin magana mai gaskiya,
da kuma cikin ikon Allah. Muna riƙe da makaman adalci dama da hagu, 8 ta wurin
ɗaukaka da ƙasƙanci, da cikin ɓata suna, da kuma cikin yabo. Cikin faɗin gaskiya,
an ɗauke mu masu ƙarya, 9 mu sanannu ne, duk da haka an ɗauke mu kamar ba a
san mu ba, muna mutuwa, duk da haka a raye muke, an ba mu horo, duk da haka
ba a kashe mu ba, 10 cikin baƙin ciki, duk da haka kullum cikin murna muke. Cikin
matalauta, duk da haka muna azurtar da mutane da yawa. Ba mu da kome, alhali
kuwa kome namu ne.
11 Ya ku Korintiyawa, mun yi muku magana a sake, muka kuma saki zuciya da ku
ƙwarai. 12 Ba mu ƙi nuna muku ƙaunarmu ba, sai dai ku kuka ƙi nuna mana. 13 A
wannan zance kam, ina magana da ku kamar 'ya'yana, ku ma ku saki zuciya da mu.

*Kada ku haɗa kai da marasa bi*

14 Kada ku haɗa kai da marasa bi. Gama me ya haɗa adalci da mugunta? Ko kuwa
me ya haɗa haske da duhu? 15 Wace daidaituwa ce tsakanin Kiristi da Iblis? Me ya
haɗa mai bi da marar bi? 16 Wane alkawari ne tsakanin haikalin Allah da na gumaka?
Gama mu haikalin Allah mai rai ne. Kamar yadda Allah ya ce,
"Zan zauna tare da su,
in yi tafiya a cikinsu,
zan zama Allahnsu,
su kuma za su zama mutanena."†
17 Saboda haka,
"Sai ku fito daga cikinsu,
ku keɓe kanku,
in ji Ubangiji.
Kada ku taɓa wani abu marar tsabta,
zan kuma karɓe ku."‡
18 Kuma,
"Zan zama Uba a gare ku,
ku kuma za ku zama 'ya'yana, maza da mata,
in ji Ubangiji Maɗaukaki."§

# 7

1 Da yake muna da waɗannan alkawura, ya ku ƙaunatattu, sai mu tsarkake kanmu
daga kowane abu da yake ƙazantar da jiki, da ruhu, mu zama da cikakken tsarki,
saboda bangirma ga Allah.

*Farin cikin Bulus*

* **6:2** Ish 49.8 † **6:16** Fir 26.12; Irm 32.38; Ezk 37.27 ‡ **6:17** Ish 52.11; Ezk 20.34,41 § **6:18** 2Sam 7.14; 2Sam 7.8

2 Ku saki zuciya da mu. Ba mu yi wa kowa laifi ba, ba mu ɓata kowa ba, ba mu
cuci kowa ba. 3 Ba na faɗin wannan don in sa muku laifi. Na riga na gaya muku
yadda muke ƙaunarku ƙwarai cikin zukatanmu, har babu abin da zai iya raba ku da
ƙaunarmu, ko a mutuwa ko a rayuwa. 4 Na amince da ku gaya, ina kuma taƙama da
ku ƙwarai. Na ƙarfafa sosai. Duk da wahalce wahalcenmu dai ina farin ciki ƙwarai
da gaske.
5 Gama sa'ad da muka zo Makidoniya, jikin nan namu bai sami hutu ba, sai ma aka
matsa mana a ta kowane gefe, a waje ga rikici, a zukatanmu kuma ga tsoro. 6 Amma
Allah, wanda yakan yi wa masu ɓacin rai ta'aziyya ya yi mana ta'aziyya da zuwan
Titus, 7 ba ma don zuwansa kaɗai ba, har ma a game da ƙarfafa zuciyan nan da
ya samu a wurinku. Ya gaya mana yadda kuke so ku gan ni sosai, da kuma yadda
kuka yi baƙin ciki game da abin da ya faru, da niyyar da kuka yi na goyon bayana.
Wannan ne ya sa na ji daɗi ƙwarai.
8 Ko da na ɓata muku rai ta wurin wasiƙata, ba na baƙin ciki da haka. Ko da yake
dā kam na yi baƙin ciki, don na lura wasiƙata ta ɓata muku rai, amma na ɗan lokaci
ne kawai. 9 Duk da haka, yanzu ina farin ciki, ba don na sa ku baƙin ciki ba, sai dai
domin baƙin cikinku ya kai ku ga tuba. Gama kun yi baƙin ciki kamar yadda Allah ya
so, saboda haka, ba ku yi hasarar kome a sanadinmu ba. 10 Baƙin ciki irin na tsoron
Allah yana kai ga tuban da yake kawo ceto, ba ya kuma kawo baƙin ciki, amma baƙin
ciki irin na duniya yakan kawo mutuwa. 11 Ku dubi abin da wannan baƙin ciki irin
na tsoron Allah ya kawo muku mana, ya sa ku marmarin aikatawa, da nuna cewa
kun yi kuskure, ya sa kuka yi fushi, kuka kuma ji tsoro, ya sa kuka sa zuciya, kuka
kuma sa aniya, ya sa kuna a shirye ku ga an yi horon da ya dace. Game da wannan
sha'ani kam, lalle ta kowace hanya kun nuna cewa ba ku da laifi. 12 To, ko da yake na
rubuta muku, ba musamman a kan wanda ya yi laifin ba ne, ba kuwa a kan wanda
aka cutar ba, sai dai domin a bayyana muku a gaban Allah tsananin kula da kuke yi
mana. 13 Ta wurin wannan duka, muka sami ƙarfafawa.
Ban da ƙarfafawar da muka samu, mun ji daɗi ƙwarai saboda yadda muka ga farin
cikin Titus, domin ruhunsa ya sami wartsakewa daga gare ku duka. 14 Na yi taƙama
da ku a wurinsa, ba ku kuwa ba ni kunya ba. Kamar dai yadda dukan abin da muka
gaya muku gaskiya ne, haka ma taƙamarmu a kanku a gaban Titus ya zama gaskiya.
15 Kaunar da yake yi muku ya ƙaru ƙwarai, duk sa'ad da yake tunawa da biyayyarku
duka, da kuma irin yawan bangirman da kuka nuna masa lokacin da kuka karɓe shi.
16 Ina farin ciki ne don na amince da ku ƙwarai da gaske.

# 8

*An ƙarfafa bayarwa*

1 To, 'yan'uwa, muna so ku san abin da alherin Allah ya ba wa ikkilisiyoyin
Makidoniya. 2 Gama sun sha wuya sosai saboda tsananin wahalar da suka shiga,
har yawan farin cikinsu ya kai su ga yin alheri ta bayarwa ga waɗansu, ko da yake
suna cikin tsananin talauci. 3 Gama ina shaida cewa sun bayar daidai gwargwadon
iyawarsu, har ma fiye da ƙarfinsu. Su kansu, 4 sun roƙe mu sosai don su sami damar
yin bayarwa a wannan hidima ga tsarkaka. 5 Ba su yi yadda muka za tă ba, sai ma
suka fara ba da kansu ga Ubangiji, sa'an nan sai suka ba da kansu gare mu bisa ga
nufin Allah. 6 Ganin haka sai muka roƙi Titus, da yake shi ne ya riga ya tsiro da
wannan aikin alheri a cikinku, sai yă ƙarasa shi. 7 To, da yake kun fiffita a kowane
abu cikin bangaskiya, cikin magana, cikin sani, cikin dukan ƙwazo, da kuma cikin
ƙaunarku dominmu, sai ku fiffita a wannan aikin alheri ma.
8 Ba umarni nake ba ku ba, sai dai ina so in gwada gaskiyar ƙaunarku ne, ta wurin
kwatanta ta da aniyar waɗansu. 9 Gama kun san alherin Ubangijinmu Yesu Kiristi

cewa ko da yake shi mawadaci ne, duk da haka, ya zama matalauci saboda ku, domin
ta wurin talaucinsa, ku zama mawadata.
[10] Ga shawarata a kan abin da ya fi muku kyau a wannan al'amari. Bara ku kuka
fara bayarwa, kuka kuma zama na farko wajen niyyar yin haka. [11] Yanzu sai ku
ƙarasa aikin da irin niyyar da kuka fara, ku yi haka gwargwadon ƙarfinku. [12] Gama
in da niyyar bayarwa, za a karɓi bayarwa bisa ga abin da mutum yake da shi, ba
bisa ga abin da ba shi da shi ba.
[13] Ba nufi nake yi a sawwaƙe wa waɗansu, ku kuwa a jibga muku nauyin ba. Amma
ya yi kyau dai [14] a raba daidai wa daida, sai ku taimake su a yanzu da yalwarku
saboda rashinsu. Wata rana su ma su taimake ku da yalwarsu saboda rashinku, don
a daidaita al'amari, [15] kamar yadda yake a rubuce cewa, "Wanda ya tara da yawa,
bai tara fiye da bukatarsa ba, wanda kuma ya tara kaɗan, bai kāsa masa ba."*

### *An aika Titus zuwa Korint*

[16] Ina gode wa Allah, wanda ya sa a zuciyar Titus, irin kula da nake da shi dominku.
[17] Ba kawai ya yarda yă je wurinku kamar yadda muka roƙe shi yă yi ba, amma ya so
yă zo kamar yadda ya riga ya yi niyya. [18] Ga shi mun aiko ɗan'uwanmu nan tare da
shi, wanda ikkilisiyoyi duka suna yabo saboda hidimarsa ga bishara. [19] Ba kuwa haka
kaɗai ba, har ma ikkilisiyoyi sun zaɓe shi yă riƙa tafiya tare da mu kan wannan aikin
alheri da muke yi saboda ɗaukakar Ubangiji, da kuma nuna kyakkyawar niyyarmu.
[20] Muna gudu kada wani yă zarge mu, a kan yadda muke gudanar da wannan kyautar
da aka bayar hannu sake. [21] Gama muna iya ƙoƙari mu yi abin da yake daidai, ba a
gaban Ubangiji kaɗai ba, amma a gaban mutane ma.
[22] Ban da wannan kuma, mun aiko da ɗan'uwanmu tare da su, wanda ya sha
tabbatar mana da ƙwazonsa ta hanyoyi iri-iri, musamman yanzu, domin ya amince
da ku da gaske. [23] Game da Titus kuma, shi abokin tarayyata ne, da kuma abokin
aikina a cikinku; game da 'yan'uwanmu kuwa, su wakilai ne na ikkilisiyoyi, kuma
su masu ɗaukaka Kiristi ne. [24] Saboda haka, ku nuna wa waɗannan mutane shaidar
ƙaunarku, da kuma dalilin taƙamarmu da ku, domin ikkilisiyoyi su gani.

## 9

[1] Babu wata bukata in rubuta muku game da hidiman nan ga tsarkaka. [2] Gama na
san aniyarku na yin taimako, ina kuma taƙama a kan wannan ga Makidoniyawa, ina
faɗin musu cewa tun bara, ku da kuke a Akayya a shirye kuke ku bayar. Koƙarinku
kuwa ya zuga yawancinsu ga aiki. [3] Amma ina aika 'yan'uwan nan don kada taƙamar
da muke yi da ku, a kan wannan al'amari ta zama a banza, sai dai domin yă zama
kuna nan a shirye, kamar yadda na faɗa za ku kasance. [4] Gama in waɗansu mutanen
Makidoniya sun zo tare da ni, suka tarar ba a shirye kuke ba, kunya ta ishe mu,
balle fa ku, saboda amincewa da muke yi da ku. [5] Saboda haka, na ga ya dace in
roƙi 'yan'uwan nan su ziyarce ku kafin lokacin, su kuma gama shirye-shirye saboda
bayarwa ta yardar ran da kuka yi alkawari. Ta haka bayarwar za tă zama a shirye,
ta yardar rai ba ta dole ba.

### *Shukin yardar rai*

[6] Ku tuna fa, duk wanda ya yi shuki kaɗan zai girbe kaɗan, kuma duk wanda ya yi
shuki da yawa, zai girbe a yalwace. [7] Ya kamata kowa yă bayar bisa ga abin da ya yi
shawara a zuciyarsa, ba tare da jin nauyi ko don dole ba, gama Allah yana son mai
bayarwa da daɗin rai. [8] Allah kuwa yana da iko yă ba ku fiye da bukatarku, domin
kullum ku wadata da kome ta kowace hanya, kuna ta bayarwa hannu sake, kowane
irin kyakkyawan aiki. [9] Kamar yadda yake a rubuce cewa,

* **8:15** Fit 16.18

"Ya ba gajiyayyu hannu sake,
ayyukansa na alheri madawwama ne."*
[10] To, shi da yake ba mai shuka iri, yake kuma ba da abinci a ci, shi ne zai ba ku irin
shukawa, yă riɓanya shi, yă kuma albarkaci ayyukanku na alheri da yawa. [11] Za a
wadatar da ku ta kowace hanya, domin ku riƙa bayarwa hannu sake a kowane lokaci.
Ta wurinmu kuma bayarwarku hannu sake za tă zama sanadin godiya ga Allah.
[12] Wannan hidimar da kuke yi, ba bukatun mutanen Allah kaɗai take biya ba,
amma tana cike da hanyoyin nuna godiya masu yawa ga Allah. [13] Aikin nan naku
na alheri tabbatar bangaskiyarku ne, za a kuwa ɗaukaka Allah saboda kun bayyana
yarda, cewa kun yi na'am da bisharar Kiristi, saboda kuma gudummawa da kuka yi
musu da saura duka, hannu sake. [14] A cikin addu'arsu dominku kuwa, zukatansu
za su koma gare ku, saboda mafificin alherin da Allah ya ba ku. [15] Godiya ga Allah,
saboda kyautarsa da ta wuce misali!

# 10

*Bulus ya kāre aikinsa*

[1] Ni Bulus da kaina, ina roƙonku albarkacin tawali'u da sanyin hali na Kiristi, ni da
ake yi wa kirari "marar tsanani" a cikinku, amma "mai matsawa" sa'ad da nake rabe
da ku! [2] Ina roƙonku cewa sa'ad da na zo kada ku tilasta ni in matsa muku, gama
na tabbata zan iya tsaya wa waɗanda suka ce abin da muke yi sha'anin duniya ne.
[3] Ko da yake muna cikin duniya, ba ma yaƙi kamar yadda duniya take yi. [4] Makaman
da muke yaƙi da su, ba makamai na duniya ba ne. Sai dai na ikon Allah ne, masu
rushe wuraren mafaka masu ƙarfi. [5] Muna ka da masu gardama da kowane tunanin
ɗaga kai da yake kafa kansa gāba da sanin Allah, muna kuma jan hankalin kowa ga
bautar Kiristi. [6] A shirye muke mu hori kowane rashin biyayya, sa'ad da biyayyarku
ta cika.
[7] Kuna duban abubuwa bisa-bisa ne kawai. In wani ya ganin cewa shi na Kiristi ne,
ya kamata yă sāke lura cewa kamar yadda yake na Kiristi, haka mu ma muke. [8] Ko
da zan yi gadara fiye da kima a game da izinin nan namu, wanda Ubangiji ya bayar
saboda inganta ku, ba don rushe ku ba, ba ni da abin jin kunya a ciki. [9] Ba na so yă
zama kamar ina ƙoƙari in tsorata ku ne da wasiƙuna. [10] Gama waɗansu suna cewa,
"Wasiƙunsa suna da nauyi da kuma ƙarfi, amma kuwa in ka gan shi, ba shi da wani
kwarjini, maganarsa kuma ba kome ba ce." [11] Ya kamata irin waɗannan mutane su
gane cewa abin da muke faɗa a cikin wasiƙunmu sa'ad da ba ma nan tare da ku, shi
muke aikatawa sa'ad da muke nan.
[12] Ba za mu yi ƙarfin halin lissafta kanmu, ko mu kwatanta kanmu da waɗansu
masu yabon kansu ba. Sa'ad da suke gwada kansu da kansu, da kuma kwatanta
kansu da kansu, ba su da hikima. [13] Amma mu kam, ba za mu yi taƙama mu zarce
iyakarmu ba, sai dai za mu yi taƙama cikin filin da Allah ya ƙayyade mana, filin kuwa
ya kai har zuwa wurinku. [14] Ba mu wuce gona da iri a taƙamarmu ba, kamar yadda
zai zama, da a ce ba mu zo wurinku ba, gama mun kai har wurinku da bisharar
Kiristi. [15] Fahariyarmu ba fiye da yadda ya kamata take ba, ba tă kuma shafi aikin
waɗansu ba. Sai dai muna sa zuciya bangaskiyarku ta riƙa ƙaruwa, ta haka kuma
fagen aikinmu a cikinku yă riƙa ƙaruwa ƙwarai da gaske. [16] Saboda mu iya yin
wa'azin bishara a yankunan da suke gaba da ku. Gama ba ma so mu yi taƙama game
da aikin da aka riga aka yi a sashen wani. [17] Amma, "Duk mai yin taƙama, sai ya
yi taƙama da Ubangiji." [18] Ai, ba mai yabon kansa ake amincewa da shi ba, sai dai
wanda Ubangiji ya yaba wa.

* **9:9** Zab 112.9

# 11

*Bulus da manzannin ƙarya*

1 Ina fata za ku yi haƙuri da ʼyar wautata. Amma, ai, kun riga kun yi haƙuri. 2 Ina
kishinku da kishi irin na Allah. Na yi muku alkawarin aure ga miji ɗaya, Kiristi,
domin in miƙa ku a gare shi kamar budurwa zalla. 3 Sai dai ina tsoro kada yǎ
zama, kamar yadda maciji ya yaudari Hawwaʼu da makircinsa, ku ma a bauɗar
da hankalinku daga sahihiyar biyayya amintacciya ga Kiristi. 4 Gama in wani ya
zo wurinku yana waʼazin wani Yesu dabam da wanda muka yi waʼazinsa, ko kuma
in kun karɓi wani ruhu dabam da wanda kuka karɓa, ko wata bishara dabam da
wadda kuka karɓa, ya nuna kun yarda da su ke nan cikin sauƙinkai. 5 Amma a
ganina waɗancan da kuke ce da su “manyan manzanni” ba su fi ni da wani abu ba.
6 Mai yiwuwa ni ba horarre ba ne a magana, amma ina da sani. Mun kuwa bayyana
muku wannan a sarari, ta kowace hanya.

7 Laifi ke nan ne na yi da na ƙasƙantar da kaina, don a ɗaga ku zuwa babban
matsayi ta wurin yin muku waʼazin bisharar Allah kyauta? 8 Na yi wa waɗansu
ikkilisiyoyi ƙwace ta wurin karɓar taimako daga wurinsu, domin in yi muku hidima.
9 Saʼad da nake tare da ku kuma nake zaman rashi, ban nawaita wa kowa ba, gama
ʼyanʼuwan da suka zo daga Makidoniya sun biya bukata. Na kiyaye kaina daga
nawaita muku ta kowace hanya, zan kuma ci gaba da yin haka. 10 Ba shakka, kamar
yadda gaskiyar Kiristi take a cikina, babu wani a yankunan Akayya da zai iya hana
yin taƙaman nan tawa. 11 Don me? Don ba na ƙaunar ku ne? Allah dai ya sani ina
ƙaunarku!

12 Zan kuma ci gaba da yin abin da nake yi, domin in toshe kafar mutanen nan
da suke fariya, suna nema mu daidaita da su. 13 Gama irin waɗannan mutane
manzannin ƙarya ne, maʼaikata ne masu ruɗi, sun ɓad da kamanni kamar su
manzannin Kiristi ne. 14 Ba abin mamaki ba ne, gama Shaiɗan kansa ma yana ɓad
da kamanni kamar shi malaʼikan haske ne. 15 Don haka, ba abin mamaki ba ne, in
bayin Shaiɗan sun ɓad da kamanni kamar su bayin adalci ne. A ƙarshe, za a sāka
musu gwargwadon ayyukansu.

*Bulus ya yi taƙama game da wahalarsa*

16 Ina sāke faɗa, kada wani yǎ ɗauka ni wawa ne. Amma in kun ɗauke ni haka,
to, sai ku karɓe ni kamar yadda kuke karɓan wawa, domin in ɗan in yi taƙama. 17 A
wannan taƙamata ba na magana yadda Ubangiji zai yi ba ne, sai dai magana ce irin
ta wawa. 18 Da yake mutane da yawa suna taƙama irin ta duniya, ni ma haka zan yi.
19 Ku kam kuna da wayo sosai, har kuna jimre wa wawaye da murna! 20 Gaskiyar
ita ce, kuna haƙuri da duk wanda ya sa ku bauta ko ya cuce ku ko ya more ku ko ya
nuna muku isa ko kuma ya mare ku a fuska. 21 Ina jin kunya in ce mun nuna kāsawa
da ba mu yi waɗannan abubuwan ba!

Abin da wani yake da ƙarfin hali yin taƙama a kai, shi ne ni ma nake ƙarfin hali
yin taƙama a kai. Ina magana kamar wawa ne. 22 In su Ibraniyawa ne, ni ma haka.
In su Israʼilawa ne, ni ma haka. In su zuriyar Ibrahim ne, ni ma haka. 23 In su bayin
Kiristi ne, ni na fi su ma, ina magana kamar ruɗaɗɗe ne fa! Ai, na fi su shan fama
ƙwarai da gaske, da shan dauri, na sha dūka marar iyaka, na sha hatsarin mutuwa
iri-iri. 24 Sau biyar Yahudawa suka yi mini bulala arbaʼin ɗaya babu. 25 Sau uku aka
bulale ni da bulalar ƙarfe, sau ɗaya aka jajjefe ni da duwatsu, sau uku jirgin ruwa
ya ragargaje ina ciki, na kwana na kuma yini ruwan teku yana tafiya da ni. 26 Na
yi tafiye-tafiye da yawa, na sha hatsari a koguna, na sha hatsarin ʼyan fashi, na sha
hatsari a hannun kabilarmu, na sha hatsari a hannun alʼummai, na sha hatsari a
birane, na sha hatsari a jeji, na sha hatsari a teku, na kuma sha hatsarin ʼyanʼuwa

na ƙarya. 27 Na yi fama, na shan wuya, ga kuma rashin barci sau da yawa. Na san
abin da ake nufin da jin yunwa da ƙishirwa, sau da yawa kuwa na kasance da rashin
abinci, na sha sanyi da zaman tsirara. 28 Ban da waɗannan abubuwa, kowace rana
ina ɗauke da nauyin kula da dukan ikkilisiyoyi. 29 Wane ne ya rasa ƙarfi, da ban ji
shi a jikina ba? Wane ne ya fāɗi cikin zunubi, da ban ji zafin wannan ba?

30 In ma lalle ne in yi taƙama, to, sai in yi taƙama da abubuwan da suka nuna rashin
ƙarfina. 31 Allah Uban Ubangiji Yesu Kiristi, wanda yabo ta tabbata a gare shi har
abada, ya san cewa ba ƙarya nake yi ba. 32 A Damaskus, gwamnan da yake ƙarƙashin
Sarki Aretas, ya sa tsare ƙofofin birnin Damaskus, don yă kama ni. 33 Amma aka
saukar da ni cikin kwando ta tagar katanga, na kuɓuce masa.

# 12

### *Wahayin Bulus da ƙayarsa*

1 Dole in ci gaba da yin taƙama. Ko da yake ba za tă amfane ni ba, zan yi magana
a kan ru'uyoyi da wahayoyi waɗanda na karɓa daga Ubangiji. 2 Na san wani a cikin
Kiristi wanda shekaru goma sha huɗu da suka wuce an ɗauke zuwa sama ta uku.
Ko a cikin jiki ne, ko kuwa ba a cikin jiki ba, ni dai ban sani ba, Allah ne ya sani.
3 Na kuma san cewa wannan mutum, ko a cikin jiki ne, ko kuma ba a cikin jiki ba,
ni dai ban sani ba, amma Allah ne ya sani, 4 an ɗauke shi ne zuwa aljanna. Ya ji
waɗansu abubuwa waɗanda ba zai iya faɗarsu da kalmomi ba, abubuwan da ba a
ba wa mutum damar faɗi. 5 Zan yi taƙama game da mutum irin wannan, sai dai ni
ba zan yi taƙama da kaina ba, sai dai a kan rashin ƙarfina. 6 Ko da zan so yin gadara
ma, ba zan zama wawa ba, gama gaskiya zan faɗa. Amma na bar zancen haka, don
kada wani ya ɗauke ni fiye da yadda yake ganina, ko yadda yake jin maganata. 7 Don
kada in cika da girman kai saboda waɗannan mafifitan manyan wahayoyi, sai aka sa
mini wata ƙaya a jikina wadda ta zama ɗan saƙon Shaiɗan, don ta wahalshe ni. 8 Sau
uku na roƙi Ubangiji yă raba ni da wannan abu. 9 Amma ya ce mini, "Alherina ya
ishe ka, domin a cikin rashin ƙarfi ne ake ganin cikar ikona." Saboda haka, zan ƙara
yin taƙama da farin ciki game da rashin ƙarfina, domin ikon Yesu Kiristi yă zauna
tare da ni. 10 Shi ya sa nake murna cikin rashin ƙarfi, da zagi, da shan wahaloli, da
tsanantawa, da matsaloli, saboda Kiristi. Don a sa'ad da nake marar ƙarfi a nan ne
nake da ƙarfi.

### *Damuwar Bulus domin Korintiyawa*

11 Na yi wauta kam, amma ku ne kuke tilasta mini, ku ne kuwa ya kamata ku yaba
mini, domin ba inda na kāsa waɗannan mafiffitan manzanni, ko da yake ni ba kome
ba ne. 12 Abubuwan da suke tabbatar da manzo, alamu, abubuwa da kuma ayyukan
banmamaki, an aikata su a cikinku da matuƙar nacewa. 13 Ta yaya ne darajarku ba
tă kai ta sauran ikkilisiyoyi ba, ko kuwa don dai ban nawaita muku ba ne? Ku gafarta
mini wannan laifi!

14 Yanzu a shirye nake in ziyarce ku sau na uku, ba zan kuma nawaita muku ba,
don ba kayanku nake so ba, ku nake so. Gama ba yara ne da ɗaukar nauyin iyayensu
ba, sai dai iyaye ne da ɗaukar nauyin yaran. 15 Don haka ina farin ciki in kashe dukan
abin da nake da shi a kanku, har in ba da kaina ma dominku. In na ƙaunace ku fiye
da haka, za ku rage ƙaunarku gare ni ne? 16 To, shi ke nan, ban nawaita muku ba.
Ashe, sai ku ce dabara na yi muku, na shawo kanku ta hanyar yaudara! 17 Na cuce
ku ne ta wurin wani daga cikin waɗanda na aiko a gare ku? 18 Na roƙi Titus ya zo
wurinku. Na kuma aiki ɗan'uwanmu tare da shi. Ko Titus ya cuce ku ne? Ba ruhu
ɗaya yake bi da mu ba? Ba kuma hanya guda muka bi ba?

19 Ko tun dā can, kuna tsammani muna kāre kanmu a gare ku ne? A gaban Allah
muke magana, kamar waɗanda suke cikin Kiristi. Kaunatattuna, kome da muke yi,
muna yi ne don inganta ku ne. 20 Gama ina tsoro, in na zo, in tarar da ku dabam
da yadda nake so, ku ma ku tarar da ni dabam da yadda kuke so. Ina tsoro kada
yă zama akwai faɗa, da kishi, da fushi mai zafi, da tsattsaguwa, da ɓata suna, da
gulma, da girman kai, da hargitsi. 21 Ina tsoro kada sa'ad da na sāke zuwa, Allahna
zai ƙasƙantar da ni a gabanku, kuma in yi baƙin ciki saboda waɗanda suka yi zunubi
a dā, ba su kuma tuba daga aikin ƙazanta, da na fasikanci, da kuma lalata da suka
sa kansu a ciki ba.

# 13

### *Gargaɗin ƙarshe*

1 Wannan za tă zama ziyarata ta uku a wurinku ke nan. "Dole a tabbatar da kowace
magana ta bakin shaidu biyu ko uku."* 2 Na riga na yi muku gargaɗi sa'ad da nake
tare da ku a zuwana na biyu. Yanzu da ba na nan tare da ku, ina maimaita irin
gargaɗin nan domin in na zo ba wanda zai kuɓuce wa horon nan, 3 da yake kuna
neman tabbaci cewa Kiristi yana magana ta wurina ne. To, ai, shi ba rarrauna ba
ne a gare ku, amma ƙaƙƙarfa ne a cikinku. 4 Ko da yake tabbatacce an gicciye shi
cikin rashin ƙarfi, duk da haka, yana rayuwa bisa ga ikon Allah. Haka mu ma marasa
ƙarfi ne a cikinsa, amma ta wurin ikon Allah za mu rayu tare da shi don mu yi muku
hidima.
5 Ku gwada kanku ku gani ko kuna cikin bangaskiya; ku auna kanku. Ashe, ba ku
san cewa Kiristi Yesu yana cikinku ba? Sai ko in kun fāɗi gwajin. 6 Ina fata za ku
gane cewa ba mu fāɗi gwajin ba. 7 Muna addu'a ga Allah kada ku aikata wani laifi.
Ba don mutane su gani cewa mun ci gwajin ba ne, a'a, sai dai don ku yi abin da yake
daidai, ko da yake zai zama kamar mun fāɗi gwajin ne. 8 Kai, ba dama mu saɓa wa
gaskiya, sai dai mu bi bayan gaskiyar. 9 Murna muke sa'ad da ba mu da ƙarfi, ku
kuwa kuna da ƙarfi. Addu'armu ita ce, ku zama cikakku. 10 Shi ya sa nake rubuta
waɗannan abubuwa, sa'ad da ba na nan tare da ku, domin sa'ad da na zo, kada yă
zama mini tilas in yi muku tsanani a game da nuna ikon nan da Ubangiji ya ba ni
saboda ingantawa, ba saboda rushewa ba.

### *Gaisuwa ta ƙarshe*

11 A ƙarshe 'yan'uwa, sai wata rana. Ku yi ƙoƙari ku zama cikakku. Ku saurari
roƙona, ku zama da tunani ɗaya, ku yi zaman salama. Allah na ƙauna da salama
kuwa zai kasance tare da ku.

12 Ku gaggai da juna da sumba mai tsarki.
13 Dukan tsarkaka suna gaishe ku.

14 Alherin Ubangiji Yesu Kiristi, da ƙaunar Allah, da zumuntar Ruhu Mai Tsarki su
kasance tare da ku duka.

* **13:1** M Sh 19.15

# Galatiyawa

1 Bulus manzo, aikakke ba daga wurin mutum ba, ba kuma ta wurin mutane ba,
amma ta wurin Yesu Kiristi da kuma Allah Uba, wanda ya tā da Yesu daga matattu.
2 Dukan ʼyanʼuwan kuma da suke tare da ni a nan,

Suna gai da ikkilisiyoyi a Galatiya.

3 Alheri da salama daga Allah Ubanmu da Ubangiji Yesu Kiristi, su kasance tare da
ku. 4 Shi wanda ya ba da kansa saboda zunubanmu don yǎ cece mu daga wannan
mugun zamani na yanzu, bisa ga nufin Allah wanda yake kuma Ubanmu, 5 a gare shi
ɗaukaka ta tabbata har abada abadin. Amin.

*Babu wata bishara*

6 Ina mamaki yadda kuka yi saurin yashe wanda ya kira ku ta wurin alherin Kiristi,
kuna juyewa ga wata bishara dabam 7 wadda a gaskiya ba bishara ba ce ko kaɗan.
Tabbatacce waɗansu mutane suna birkitar da ku, suna kuma ƙoƙari su karkatar da
bisharar Kiristi. 8 Amma ko mu, ko malaʼika daga sama ya yi waʼazin wata bishara
dabam da wadda muka yi muku, bari yǎ zama laʼananne har abada! 9 Kamar yadda
muka riga muka faɗa, haka yanzu ma ina ƙara cewa in wani yana muku waʼazin
wata bishara dabam da wadda kuka karɓa, bari yǎ zama laʼananne har abada!
10 Za a ce, ina ƙoƙarin neman amincewar mutane ne, ko amincewa ta Allah? Ko
kuwa ina ƙoƙarin faranta wa mutane zuciya ne? Da a ce har yanzu ina ƙoƙarin
faranta wa mutane zuciya ne, ai, da ban zama bawan Kiristi ba.

*Bulus kirayaye na Allah*

11 Ina so ku sani ʼyanʼuwa, cewa bisharar da nake waʼazi, ba mutum ne ya ƙago
ta ba. 12 Ban karɓe ta daga wurin wani mutum ba, ba a kuma koya mini ita ba, a
maimako, na karɓe ta, ta wurin wahayi daga Yesu Kiristi ne.
13 Kun dai ji labarin rayuwata ta dā a cikin Yahudanci, yadda na tsananta wa
ikkilisiyar Allah ƙwarai, na kuma yi ƙoƙarin hallaka ta. 14 Na ci gaba a cikin
Yahudanci fiye da yawancin Yahudawan da suke tsarana, na kuma yi ƙwazo ƙwarai
ga bin alʼadun kakannina. 15 Amma saʼad da Allah, wanda ya keɓe ni daga mahaifa*
ya kira ni ta wurin alherinsa, ya kuma gamshe shi 16 yǎ bayyana Ɗansa a cikina,
domin in yi waʼazinsa cikin Alʼummai. Ban nemi shawarar wani mutum ba. 17 Ban
kuma tafi Urushalima domin in ga waɗanda suka riga ni zaman manzanni ba, sai
dai na hanzarta na tafi ƙasar Arabiya, daga baya sai na koma Damaskus.
18 Bayan shekara uku, sai na haura zuwa Urushalima domin in sadu da Bitrus†, na
kuwa zauna tare da shi kwana goma sha biyar. 19 Ban ga wani a ciki sauran manzanni
ba, sai dai Yaƙub ɗanʼuwan Ubangiji. 20 Ina tabbatar muku a gaban Allah cewa abin
da nake rubuta muku ba ƙarya ba ne.
21 Daga baya sai na tafi Suriya da Silisiya. 22 Ikkilisiyoyin da suke cikin Kiristi da
suke a Yahudiya ba su san ni ba tukuna. 23 Sun dai sami labari ne kawai cewa,
“Mutumin da dā yake tsananta mana yanzu yana waʼazin bangaskiyar da dā ya yi
ƙoƙari yǎ hallaka.” 24 Sai suka yabi Allah saboda ni.

* **1:15** Ko kuwa daga cikin mahaifiyata † **1:18** Girik Kefas

# 2

### *Manzanni sun karɓi Bulus*

1 Bayan shekara goma sha huɗu sai na sāke haurawa zuwa Urushalima, a wannan
lokaci na tafi tare da Barnabas. Na kuma ɗauki Titus muka tafi tare. 2 Na tafi ne bisa
ga wani wahayi. Da na kai can, sai na bayyana musu bisharar da nake waʼazi a cikin
Alʼummai. Na yi haka a keɓance a gaban waɗanda suke shugabanni, don tsoro kada
gudun da nake yi, ko kuwa na riga na yi, yǎ zama a banza. 3 Amma ko Titus ma da
yake tare da ni, ba a ce dole sai ya yi kaciya ba, ko da yake shi mutumin Alʼummai ne.
4 Wannan zancen kaciya ya taso domin waɗansu ʼyanʼuwan ƙarya sun shiga cikinmu
domin su yi leƙe a kan ʼyancin da muke da shi a cikin Kiristi Yesu, su kuma mai da
mu bayi. 5 Ba mu kuwa ba su zarafi ba ko kaɗan, don gaskiyar bishara ta ci gaba da
kasance tare da ku.
6 Game da waɗanda aka ɗauka a dā a kan su wani abu ne, ko wane ne su, duk
ɗaya ne a wurina; gama Allah ba ya nuna bambanci, ina dai gaya muku waɗannan
da suke wani abu ne a dā, ba su ƙara mini kome ba. 7 A maimakon haka, sun
ga cewa an danƙa mini hakkin waʼazin bishara ga Alʼummai,[*] kamar yadda aka
danƙa wa Bitrus ga Yahudawa.[†] 8 Gama Allah wanda ya yi aiki a cikin hidimar Bitrus
a matsayin manzo ga Yahudawa, haka ma ya yi aiki a cikin hidimata a matsayin
manzo ga Alʼummai. 9 Yaƙub, Bitrus da Yohanna waɗanda suke fitattun ginshiƙai,
sun karɓe ni da Barnabas da hannu biyu biyu saʼad da suka gane alherin da aka ba
ni. Suka kuma yarda cewa ya kamata mu tafi wajen Alʼummai, su kuwa su tafi wajen
Yahudawa. 10 Abin da dai suka roƙa shi ne ya kamata mu riƙa tuna da matalauta,
abin nan da nake marmarin yi.

### *Bulus ya tsawata wa Bitrus*

11 Saʼad da Bitrus ya zo Antiyok, na tsawata masa ido da ido don laifinsa a fili yake.
12 Kafin waɗansu mutane su zo daga wurin Yaƙub, yakan ci abinci tare da Alʼummai.
Amma da suka iso, sai ya fara janyewa, ya kuma ware kansa daga wajen Alʼummai
domin yana tsoron waɗanda suke ƙungiyar masu kaciya. 13 Sauran Yahudawa suka
haɗa kai da shi a munafuncinsa har Barnabas ma ya bauɗe.
14 Da na ga cewa ba sa yin daidai da gaskiyar bishara, sai na ce wa Bitrus a gabansu
duka, “Kai mutumin Yahuda ne, duk da haka kana rayuwa kamar Baʼalʼumme ba
kamar mutumin Yahuda ba. To, yaya aka yi, kana tilasta Alʼummai su bi alʼadun
Yahudawa?
15 “Mu da muke Yahudawa ta wurin haihuwa ba Alʼummai masu zunubi ba, 16 mun
san cewa mutum ba ya samun kuɓuta ta wurin kiyaye Doka, sai dai ta wurin
bangaskiya cikin Kiristi Yesu. Saboda haka, mu ma, muka sa bangaskiyarmu cikin
Kiristi Yesu don mu sami kuɓuta ta wurin bangaskiya cikin Kiristi ba ta wurin kiyaye
Doka ba, domin ba wanda zai kuɓuta ta wurin bin Doka.
17 “In kuwa ya zama muna so mu sami zaman marasa laifi a gaban Allah ta wurin
dogara ga Kiristi, saʼan nan an same mu mu kanmu ma masu zunubi ne, ashe, ko
wannan zai nuna Kiristi yana ƙarfafa zunubi ke nan? Aʼa, ko kusa! 18 In na sāke
gina abin da na rushe, na zama mai karyar Doka ke nan.
19 “Gama ta wurin Doka na mutu ga Doka saboda in rayu ga Allah. 20 An gicciye ni
tare da Kiristi. Yanzu ba ni ne nake raye ba, Kiristi ne yake raye a cikina. Rayuwar da
nake yi a jiki, ina rayuwa ce ta wurin bangaskiya cikin Ɗan Allah, wanda ya ƙaunace
ni ya kuma ba da kansa domina. 21 Ba na ajiyar alherin Allah a gefe, gama da a ce
ana samun adalci ta wurin Doka, ai, da Kiristi ya mutu a banza ke nan!”

---

[*] **2:7** Girik marasa kaciya [†] **2:7** Girik masu kaciya; haka ma a ayoyi 8 da kuma 9

# 3

*Bangaskiya ko kiyaye doka*

1 Ya ku Galatiyawa marasa azanci! Wa ya ruɗe ku? A idanunku aka bayyana Yesu
Kiristi gicciyeyye a sarari. 2 Zan so in san abu guda tak daga gare ku. Kun karɓi Ruhu
ta wurin kiyaye Doka ne, ko kuwa ta wurin gaskata abin da kuka ji? 3 Ashe, rashin
azancinku har ya kai ga haka? Bayan kun fara da Ruhu, a yanzu kuma da halin
mutuntaka za ku ƙarasa? 4 Ashe, wahaloli dabam-dabam da kuka sha sun zama a
banza ke nan? Haka zai yiwu kuwa? 5 Allah ya ba ku Ruhunsa yana kuma aikata
ayyukan banmamaki a cikinku saboda kuna kiyaye Doka ne, ko kuwa domin kuna
gaskatawa abin da kuka ji ne? 6 Ku dubi Ibrahim mana, "Ya gaskata Allah, aka kuwa
lissafta wannan adalci ne a gare shi."*

7 Ku sani fa, waɗannan waɗanda suka gaskata, 'ya'yan Ibrahim ne. 8 Nassi ya
hanga cewa Allah zai kuɓutar da Al'ummai ta wurin bangaskiya, ya kuwa sanar wa
Ibrahim wannan bisharar tun kafin lokaci yă yi cewa, "Dukan al'ummai za su sami
albarka ta wurinka."† 9 Saboda haka waɗanda suke da bangaskiya sun sami albarka
tare da Ibrahim, mutumin bangaskiya.

10 Dukan waɗanda suka dogara ga kiyaye Doka la'anannu ne, gama a rubuce yake
cewa, "La'ananne ne duk wanda bai ci gaba da yi dukan abubuwan da aka rubuta
a Littafin Doka ba."‡ 11 A fili yake ba wanda zai kuɓuta a gaban Allah ta wurin
Doka, domin "Mai adalci zai rayu ta wurin bangaskiya."§ 12 Doka ba tă dangana ga
bangaskiya ba; a maimakon haka, "Mutumin da ya aikata waɗannan abubuwa zai
rayu ta wurinsu."* 13 Kiristi ya fanshe mu daga la'anar Doka ta wurin zama la'ana
saboda mu, gama a rubuce yake cewa, "La'ananne ne duk wanda aka rataye a kan
itace."† 14 Ya fanshe mu domin albarkar da aka yi wa Ibrahim yă zo ga Al'ummai, ta
wurin Kiristi Yesu, domin ta wurin bangaskiya mu karɓi alkawarin Ruhu.

*Doka da kuma alkawari*

15 'Yan'uwa, bari in yi muku misali da rayuwarmu ta yau da kullum. Kamar dai
yadda ba mai kawarwa ko yă ƙara wani abu cikin alkawarin da mutane suka kafa,
haka yake a wannan batu. 16 Alkawaran nan fa ga Ibrahim ne aka faɗa da kuma
wani zuriyarsa. Nassi bai ce, "da zuriyoyi ba" wanda ya nuna kamar mutane da
yawa, amma "ga zuriyarka,"‡ wanda yake nufin mutum ɗaya, wanda shi ne Kiristi.
17 Abin da nake nufi shi ne, Dokar da aka shigar ita bayan shekaru 430, ba tă kawar
da alkawarin da Allah ya yi tun dā ba. 18 Gama da a ce gādon yă dangana a kan doka
ne, ai, da ba zai dangana a kan alkawari ba; amma Allah cikin alherinsa ya ba wa
Ibrahim gādon ta wurin alkawari.

19 To, don me aka kawo Doka? An yi ƙari da Doka ne don fitowa da laifi fili har
kafin na zuriyan nan ya zo, wanda aka yi wa alkawarin, an ba da doka ta wurin
mala'iku ne, aka kuma danƙa ta a hannun matsakanci. 20 Kuma akan bukaci wani a
tsakani ne idan da mutum biyu ake zance, Allah kuwa ɗaya ne.

21 To, Dokar ce tana gāba da alkawaran Allah ke nan? Sam, ko kaɗan! Gama da
a ce an ba da Dokar da tana iya ba da rai, tabbatacce, da sai a sami adalci ta wurin
Doka. 22 Amma Nassi ya kulle kome a ƙarƙashin ikon zunubi, domin abin da aka yi
alkawarin nan, da ake bayar ta wurin bangaskiya a cikin Yesu Kiristi, a ba da shi ga
waɗanda suka gaskata.

*'Ya'yan Allah*

---

* **3:6** Far 15.6 † **3:8** Far 12.3; Far 18.18; Far 22.18 ‡ **3:10** M Sh 27.26 § **3:11** Hab 2.4 * **3:12** Fir 18.5
† **3:13** M Sh 21.23 ‡ **3:16** Far 12.7; Far 13.15; Far 24.7

[23] Kafin bangaskiyan nan tă zo, mun kasance a daure a kurkuku a ƙarƙashin Doka,
a kulle sai da bangaskiyar da za tă zo ta bayyana. [24] Ta haka aka sa Dokar ta zama
jagorarmu zuwa ga Kiristi don mu sami kuɓuta ta wurin bangaskiya. [25] Yanzu da
bangaskiya ta zo, ba sauran zamanmu a ƙarƙashin Doka.
[26] Dukanku ʼyaʼyan Allah ne ta wurin bangaskiya cikin Kiristi Yesu. [27] Gama
dukanku da aka yi muku baftisma cikin Kiristi, kuna sanye da Kiristi ke nan. [28] Babu
bambanci tsakanin mutumin Yahuda da mutumin Alʼummai, bawa da ʼyantacce,
namiji da ta mace, gama dukanku ɗaya ne cikin Kiristi Yesu. [29] In kuwa ku na Kiristi
ne, to, ku zuriyar Ibrahim ne, magāda kuma bisa ga alkawarin nan.

# 4

[1] Abin da nake nufi shi ne, muddin magāji yana ɗan yaro ne tukuna, babu bambanci
tsakaninsa da bawa, ko da yake shi ne da mallakar kome. [2] Yana ƙarƙashin iyayen
goyonsa da masu riƙon amana har yă zuwa cikar lokacin da mahaifinsa ya sa. [3] Haka
yake, saʼad da muke ʼyan yara, mun kasance cikin bauta a ƙarƙashin ƙaʼidodin
duniya. [4] Amma da lokacin da aka tsara ya yi sosai, sai Allah ya aiki Ɗansa, haifaffe
daga mace, haifaffe a ƙarƙashin Doka, [5] domin yă fanshi waɗanda suke a ƙarƙashin
doka, saboda mu sami cikakken matsayin zaman ʼyaʼya. [6] Da yake ku ʼyaʼya ne, sai
Allah ya aiko da Ruhun Ɗansa a cikin zukatanmu, Ruhun da yake kira, "*Abba*,* Uba."
[7] Saboda haka kai ba bawa ba ne kuma, kai ɗa ne; da yake kuwa kai ɗa ne, Allah ya
mai da kai magāji.

### *Damuwar Bulus domin Galatiyawa*

[8] Dā da ba ku san Allah ba, ku bayi ne ga waɗanda a ainihi ba alloli ba ne. [9] Amma
yanzu da kuka san Allah, ko kuma a ce Allah ya san ku, yaya kuke sāke komawa
ga ƙaʼidodin duniya marasa ƙarfi, abin tausayi kuma? Kuna so ku sāke komawa ga
bautarsu ne? [10] Kuna kiyaye ranaku da watanni da lokuta da shekaru na musamman!
[11] Kai, kun ba ni tsoro, don ya zama kamar duk wahalar da na yi a kanku banza ne!
[12] Ina roƙonku ʼyanʼuwa, ku zama kamar ni, gama na zama kamar ku. Ba ku yi
mini wani laifi ba. [13] Kun san rashin lafiyar da na yi, shi ne ya yi mini hanyar da
na kawo muku bishara da farko. [14] Ko da yake ciwona gwaji ne gare ku, ba ku yi
mini reni ko ƙyama ba. A maimakon haka, kuka karɓe ni sai ka ce malaʼikan Allah,
kuma sai ka ce Kiristi Yesu kansa. [15] Me ya faru da dukan farin cikinku? Na tabbata,
a lokacin, da mai yiwuwa ne da kun ciccire idanunku kun ba ni. [16] Yanzu na zama
abokin gābanku don na faɗa muku gaskiya ke nan?
[17] Waɗancan mutane suna neman su rinjaye ku da ƙwazo, amma ba da kyakkyawar
aniya ba. Abin da suke so shi ne su raba ku da mu, saboda ƙwazonku yă koma gare
su. [18] Yana da kyau ku kasance da irin wannan niyya idan da nufi mai kyau ne, ku
kuma kasance a haka koyaushe ba sai ina tare da ku ba. [19] Ya ku ʼyaʼyana ƙaunatattu,
ina sāke shan wahalar naƙudarku, har sai Kiristi ya kahu a cikinku. [20] Da ma a ce
ina tare da ku yanzu in canja muryata mana! Gama na damu ƙwarai saboda ku!

### *Saratu da Hagar*

[21] Ku gaya mini, ku da kuke so ku zauna a ƙarƙashin Doka, ba ku san abin da Doka
ta ce ba ne? [22] Gama a rubuce yake cewa Ibrahim yana da ʼyaʼya biyu maza, ɗaya
ta wurin mace ʼyar aikin gidansa, ɗaya kuma ta wurin ainihin matarsa. [23] Ɗansa na
wajen mace ʼyar aikin gidansa ya zo bisa ga ƙaʼidar jiki ne; amma ɗansa na wajen
ainihin matarsa ya zo a sakamakon alkawarin ne.
[24] Za a iya ɗaukan waɗannan alʼamura a matsayin misali, domin matan nan suna
misalta alkawura biyu ne. Alkawari ɗaya daga Dutsen Sinai ne yana kuma haihuwar

* **4:6** Arameyik na Mahaifi

ʼyaʼyan da za su zama bayi. Hagar ke nan. 25 Hagar tana a matsayin Dutsen Sinai
a Arabiya tana kuma kwatancin birnin Urushalima na yanzu, gama ita baiwa ce
tare da ʼyaʼyanta. 26 Amma Urushalimar da take sama ʼyantacciya ce, ita ce kuma
mahaifiyarmu. 27 Gama a rubuce yake cewa,

"Ki yi farin ciki, ya ke bakararriya,
wadda ba ta haihuwa
ki ɓarke da murna, ki kuma tā da murya,
ke da ba kya naƙuda;
domin da yawa ne ʼyaʼyan macen da aka yashe,
fiye da na mai miji."†

28 To, ku ʼyanʼuwa, ku ʼyaʼyan alkawari ne kamar Ishaku. 29 A wancan lokaci,
wannan ɗa wanda aka haifa ta wurin ƙaʼidar jiki ya tsananta wa wanda aka haifa
ta ikon Ruhu. Haka ma yake har yanzu. 30 Amma me Nassi ya ce? Nassi ya ce, "Kori
macen nan ʼyar aikin gida da ɗanta don ɗan mace ʼyar aikin gida ba zai taɓa raba
gādo tare da ɗa na ainihin matarka ba."‡ 31 Saboda haka, ʼyanʼuwa, mu ba ʼyaʼyan
mace ʼyar aikin gida ba ne, amma na ainihin matan gidan ne.

# 5

### *ʼYanci cikin Kiristi*

1 Saboda ʼyanci ne Kiristi ya ʼyantar da mu. Sai ku tsaya daram, kada ku yarda ku
sāke komawa ƙarƙashin nauyin bauta.

2 Ku lura da kalmomina! Ni Bulus ina gaya muku cewa in kuka yarda aka yi muku
kaciya, wannan ya nuna Kiristi ba shi da amfani a gare ku ba ko kaɗan. 3 Haka kuma
ina ƙara sanar wa kowane mutumin da ya yarda aka yi masa kaciya cewa dole yă
kiyaye dukan Doka. 4 Ku da kuke ƙoƙarin kuɓuta ta wurin Doka an raba ku da Kiristi
ke nan; kuka kuma fāɗi daga alheri. 5 Amma ta wurin bangaskiya muna marmarin
jira adalcin da muke bege ta wurin Ruhu. 6 Gama a cikin Kiristi Yesu, kaciya ko rashin
kaciya ba su da wani amfani. Abin da kawai yake da amfani shi ne, bangaskiyar da
take bayyana kanta ta wurin ƙauna.

7 Kun yi tsere mai kyau a dā. Wa ya shige gabanku ya hana ku bin gaskiya?
8 Wannan rarrashin da ake muku ba daga wanda ya kira ku ba ne. 9 "Dan yisti
kaɗan ne yake gama dukan curin burodi." 10 Ina da tabbaci cikin Ubangiji cewa ba
za ku bi wani raʼayi dabam ba. Wannan da yake rikita ku za a hukunta shi, ko shi
wane ne. 11 ʼYanʼuwa, da a ce har yanzu ina waʼazin kaciya ne, to, me ya sa ake
tsananta mini har yanzu? In haka ne, ashe, an kawar da abin da yake sa tuntuɓe
game da gicciye ke nan. 12 Da ma a ce masu tā da hankalinku ɗin nan su yanke
gabansu gaba ɗaya mana!

13 Ku ʼyanʼuwana, an kira ku ga zama ʼyantattu. Amma kada ku yi amfani da
ʼyancinku don aikata ayyukan mutuntaka* a maimakon haka, ku yi hidimar juna
da ƙauna. 14 Dukan doka an taƙaita a cikin umarni ɗaya ne cewa, "Ka ƙaunaci
maƙwabcinka kamar kanka."† 15 In kun ci gaba da cizo, kuna kuma cin naman juna,
ku yi hankali in ba haka ba za ku hallaka juna.

### *Rayuwa ta wurin Ruhu*

16 Saboda haka ina ce muku, ku yi rayuwa ta wurin Ruhu, ba za ku kuwa gamsar
da shaʼawace-shaʼawacen mutuntaka ba. 17 Gama mutuntaka yana son abin da Ruhu
yake ƙi, Ruhu kuma yana son abin da mutuntaka yake ƙi. Waɗannan biyu kuwa

† **4:27** Ish 54.1 ‡ **4:30** Far 21.10 * **5:13** Ko kuwa na jiki; haka ma a ayoyi 16, 17, 19 da 24 † **5:14** Fir 19.18

gāba suke da juna, har ku kāsa yin abin da kuke so. [18] Amma in Ruhu ne yake bishe
ku, ba ku a ƙarƙashin Doka ke nan.
[19] Ayyukan mutuntaka kuwa a fili suke. Wato, fasikanci, ƙazanta da kuma lalata;
[20] bautar gumaka da sihiri; ƙiyayya, faɗa, kishi, fushi mai zafi, sonkai, tsattsaguwa,
hamayya, [21] da ƙyashi; buguwa, shashanci, da ire-irensu. Na gargaɗe ku, yadda na
yi a dā, cewa masu irin wannan rayuwa ba za su gāji mulkin Allah ba.
[22] Amma amfanin da Ruhu yake bayar shi ne ƙauna, farin ciki, salama, haƙuri,
kirki, nagarta, aminci, [23] sauƙinkai, da kuma kamunkai. Ai, ba ruwan Doka da
waɗannan abubuwa. [24] Waɗanda suke na Kiristi Yesu, sun gicciye mutuntaka tare da
abubuwan da mutum yake marmari da kuma sha'awace-sha'awacensa. [25] Da yake
muna rayuwa ta Ruhu ne, bari mu ci gaba da al'amuranmu ta wurin Ruhu. [26] Kada
mu zama masu girman kai, muna tsokana muna kuma jin kishin juna.

# 6

### *Yin alheri ga kowa*

[1] 'Yan'uwa, in an kama wani yana cikin yin zunubi, ku da kuke masu ruhaniya ya
kamata ku komo da shi a kan hanya a hankali. Amma ku lura da kanku, domin kada
maimakon dawowa da ɗan'uwanku, ku ma ku fāɗi cikin jarraba. [2] Ku ɗauki nawayar
juna, a haka kuwa za ku cika dokar Kiristi. [3] In wani yana tsammani shi wani abu ne
alhali kuwa shi ba kome ba, ruɗin kansa yake yi. [4] Kowa yă auna ayyukansa. A sa'an
nan ne zai iya yin taƙama da kansa, ba tare da kwatanta kansa da wani ba, [5] gama
kowa zai ɗauki kayansa. [6] Duk haka, wanda aka koya wa maganar Kiristi, bari yă
raba abubuwan nan na alheri tare da wanda ya koyar da shi.
[7] Kada a ruɗe ku. Ba a yi wa Allah ba'a. Mutum yakan girbe abin da ya shuka
ne. [8] Wanda ya yi shuki don yă gamshi mutuntakarsa, daga wannan mutuntaka
zai girbi hallaka. Wanda ya yi shuki domin yă gamshi Ruhu, daga Ruhu zai girbi
rai madawwami. [9] Kada mu gaji da yin nagarta, gama a daidai lokaci za mu girbe
amfani, in ba mu fid da zuciya ba. [10] Saboda haka, in da hali, bari mu aikata nagarta
ga dukan mutane, musamman ga waɗanda suke na iyalin masu bi.

### *Ba kaciya ba, sai dai sabuwar halitta*

[11] Ku dubi irin manya-manyan harufan da na yi amfani da su yayinda nake rubuta
muku da hannuna!

[12] Waɗanda suke son nuna bajinta a fili suna ƙoƙari su tilasta muku ku yi kaciya
ne. Dalilin kaɗai da suke yin haka shi ne don gudu kada a tsananta musu saboda
gicciyen Kiristi ne. [13] Kai, su masu kaciya ma ba su kiyaye Doka ba, duk da haka suna
so a yi muku kaciya don su yi taƙama kan an yi muku kaciya. [14] Kada in taɓa yin
taƙama ga kome sai dai a cikin gicciyen Ubangijinmu Yesu Kiristi, wanda ta wurinsa
aka gicciye duniya a gare ni, aka kuma gicciye ni ga duniya. [15] Kaciya ko rashin
kaciya ba wani abu ba ne; abin da yake da amfani shi ne sabuwar halitta. [16] Salama
da jinƙai su tabbata ga dukan waɗanda suke bin wannan ƙa'ida, har ma ga Isra'ila
na Allah.

[17] A ƙarshe, kada kowa yă ƙara damuna, gama ina ɗauke da raunuka masu nuna
ni bawan Ubangiji Yesu ne.

[18] 'Yan'uwa! Alherin Ubangijinmu Yesu Kiristi yă kasance tare da ruhunku. Amin.

# Afisawa

[1] Bulus, wanda Allah ya zaɓa don yă zama manzon Kiristi Yesu,

Zuwa ga tsarkaka da suke a Afisa,* da kuma suke amintattu† cikin Kiristi Yesu.

[2] Alheri da salama daga Allah Ubanmu da Ubangiji Yesu Kiristi, su kasance tare da ku.

*Albarkun ruhaniya a cikin Kiristi*

[3] Yabo ya tabbata ga Allah Uban Ubangijinmu Yesu Kiristi, wanda ya kawo mana
kowace albarka ta ruhaniya daga sama. [4] Gama ya zaɓe mu a cikin Kiristi tun dā
can, kafin ma a halicci duniya don mu zama masu tsarki da kuma marasa aibi a
gabansa. [5] A cikin ƙauna, ya‡ ƙaddara mu zama 'ya'yansa na riƙo ta wurin Kiristi
Yesu, bisa ga nufinsa na alheri. [6] Ya yi haka don mu yabi Allah saboda alherin da
ya yi mana saboda mu na ƙaunataccen Ɗansa ne. [7] A cikinsa muka sami fansa ta
wurin jininsa, wato, yafewar zunubanmu. Kiristi ya yi wannan saboda yawan alherin
Allah [8] wanda ya ba mu babu iyaka tare da dukan hikima da fahimta. [9] Allah ya yi
abin da ya nufa, ya kuma sanar mana shirin asirin da ya riga ya shirya yă cika ta
wurin Kiristi. [10] Nufinsa ke nan, idan lokaci ya cika, yă harhaɗa dukan abubuwa a
ƙarƙashin ikon Kiristi, wato, dukan abubuwan da suke sama da abubuwan da suke
ƙasa.
[11] A cikinsa ne kuma aka zaɓe mu mu sami gādo daga Allah,§ an kuwa ƙaddara mu
ga haka bisa ga nufin wannan da yake zartar da dukan abubuwa yadda ya yi nufi yă
yi. [12] Manufar Allah ita ce cewa mu da muka fara sa bege a cikin Kiristi, mu yi zaman
yabon ɗaukakar Allah. [13] An kuma haɗa ku a cikin Kiristi lokacin da kuka ji saƙon
nan na gaskiya, wanda yake labari mai daɗi na cetonku. Da kuka ba da gaskiya, sai
aka yi muku alamar shaida a cikinsa da Ruhu Mai Tsarki. [14] Ruhu Mai Tsarkin nan
shi ne tabbacin da Allah ya yi na cewa zai ba mu kome da ya yi alkawari, har ya sa
muka sani nan gaba Allah zai ceci waɗanda suke nasa. Wannan kuwa domin yabon
ɗaukakarsa ne.

*Godiya da addu'a*

[15] Saboda haka, tun lokacin da na ji labarin bangaskiyarku cikin Ubangiji Yesu da
kuma ƙaunar da kuke yi wa dukan mutanen Allah, [16] ban fasa yin godiya saboda
ku ba, ina tuna da ku cikin addu'o'ina. [17] Ina ta roƙo cewa Allah na Ubangijinmu
Yesu Kiristi, Uba Maɗaukaki, yă ba ku Ruhun hikima da na ganewa, domin ku san
shi da kyau. [18] Ina kuma addu'a cewa zuciyarku tă waye don ku gane ko mene ne sa
zuciyan nan da ya kira ku a kansa, ku kuma san darajar dukiyan nan wadda take ta
mutanen Allah, wato, albarkunsa. [19] Ina addu'a ku san girman ikon Allah wanda ya
wuce misali, wanda yake namu. Ikon da yake aiki a cikinmu, ɗaya ne da ikon nan
[20] da ya tā da Kiristi daga matattu, ya kuma sa ya zauna a hannun damansa a cikin
mulkin samaniya. [21] Yanzu yana mulki a kan dukan masu sarauta, da masu iko, da
masu ƙarfi, da kuma masu mulki. Yana mulkin kome a wannan duniya, zai kuma yi
mulkin duniya mai zuwa. [22] Allah ya sa kome a ƙarƙashin ikonsa, ya kuma ba shi

* **1:1** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā ba su da a Afisa. † **1:1** Ko kuwa masu bi waɗanda ‡ **1:5** Ko kuwa gani cikin ƙauna. 5 Ya § **1:11** Ko kuwa mun zama abin gādon Allah

iko a kan kome don amfanin ikkilisiya. 23 Kuma ikkilisiya ce jikinsa; ta kuma cika da
Kiristi, wanda ya cika kome ta kowace hanya.

# 2

*An raya ku a cikin Kiristi*

1 Ku kam, a dā ku matattu ne saboda laifofinku da kuma zunubanku. 2 Kun yi
rayuwa kamar yadda sauran mutanen duniya suke yi, cike da zunubi, kuna biyayya
ga sarki masu ikon sarari sama, wato, ruhun nan da yanzu yake aiki a cikin masu
ƙin biyayya ga Allah. 3 Dukanmu a dā mun yi irin rayuwan nan a cikinsu, muna bin
kwaɗayi da sha'awace-sha'awacen jikunanmu da tunaninmu. Kamar sauran mutane,
mun cancanci fushin Allah. 4 Amma saboda yawan ƙaunar da yake mana, Allah,
wanda yake mai yawan jinƙai, 5 ya ba mu rai sa'ad da ya tashe Kiristi daga matattu.
Ta wurin alherin Allah ne aka cece ku. 6 Allah ya tashe mu tare da Kiristi, ya kuma
ba mu wurin zama tare da shi a cikin mulkin samaniya. 7 Allah ya yi haka domin
a tsararraki masu zuwa yǎ nuna yalwar alherinsa da ya wuce misali, an bayyana
alheransa da ya yi mana ta wurin Kiristi Yesu. 8 Allah ya cece ku ta wurin alheri
sa'ad da kuka ba da gaskiya. Wannan kuwa ba yinku ba ne, kyauta ce daga Allah.
9 Ba kuwa saboda aikin lada ba, don kada wani yǎ ɗaga kai. 10 Ai, mu aikinsa ne,
an sāke halittarmu a cikin Kiristi Yesu musamman domin mu yi kyawawan ayyuka,
waɗanda Allah ya tanadar mana tun da fari, mu yi.

*An sulhunta Yahudawa da al'ummai su zama ɗaya ta wurin Kiristi*

11 Saboda haka, ku tuna dā ku Al'ummai ne bisa ga haihuwa, waɗanda kuma ake
kira masu "kaciya" sukan kira ku "marasa kaciya" (ga shi kuwa, kaciyar nan ta jiki
ce, wadda ake yi da hannu). 12 Ku kuma tuna a lokacin ba ku san Kiristi ba. A ware
kuke daga mutanen Isra'ila, ba ku kuma da dangantaka da alkawaran da Allah ya yi
da su. Kun yi zama a duniyan nan babu bege kuma babu Allah. 13 Amma yanzu a
cikin Kiristi Yesu, ku da dā kuke can da nesa an kawo ku kusa ta wurin jinin Kiristi.
14 Gama shi kansa shi ne salamarmu, shi ne ya kawo ƙungiyoyi biyu suka zama
ɗaya, ya kuma rushe katangan nan ta ƙiyayya wadda ta raba mu. 15 Kiristi ya ba
da jikinsa don yǎ kawar da doka da dukan umarnanta da kuma ƙa'idodinta. Ya
yi haka domin yǎ halicci sabuwar zuriya daga zuriyoyin nan biyu. Ta haka kuma
ya kawo salama tsakaninsu. 16 A kan gicciye, Kiristi ya kawar da ƙiyayyar da take
tsakaninmu da juna. Ya kuma kawo sulhu tsakaninmu da Allah. 17 Ya zo ya yi muku
wa'azin salama; ku da kuke nesa da shi, ya kuma yi wa waɗanda suke kusa. 18 Gama
ta wurinsa dukanmu za mu iya zuwa gun Uba ta wurin Ruhu guda.
19 Don haka, yanzu ku ba baƙi ba ne, ku kuma ba bare ba ne. Ku 'yan ƙasa ne
tare da mutanen Allah, iyalin gidan Allah kuma. 20 Ku gini ne wanda manzanni da
annabawa suke tushensa, Kiristi kuma shi ne dutse mafi muhimmanci na ginin. 21 Ta
wurinsa ne dukan ginin yake a haɗe, shi ne kuma yake sa ginin yǎ yi girma, yǎ zama
haikali mai tsarki domin Ubangiji. 22 Ku ma sashe ne na wannan ginin da Kiristi ya
yi inda Allah yake zaune ta wurin Ruhunsa.

# 3

*Kyakkyawan shirin Allah domin al'ummai*

1 Saboda haka, ni Bulus, na zama ɗan kurkuku na Kiristi Yesu saboda ku Al'ummai.
2 Na tabbata kun ji labarin hidimar alheri na musamman da Allah ya ba ni dominku.
3 Wannan wasiƙa za tǎ faɗa muku kaɗan game da yadda Allah ya bayyana mini
shirinsa na asiri. 4 A yayinda kuke karanta wannan, za ku gane abin da na sani game
da wannan shirin Kiristi. 5 Ba a sanar da wannan asiri wa wani a sauran zamanai

ba, amma a yanzu an bayyana shi ta wurin Ruhu Mai Tsarki ga manzanninsa da
annabawansa. 6 Asirin nan kuwa shi ne cewa ta wurin bishara, Al'ummai sun zama
waɗanda za su yi gādo tare da Isra'ila, sun zama gaɓoɓin jiki ɗaya, abokan tarayya
kuma ga alkawaran nan a cikin Kiristi Yesu.
7 Na zama bawan wannan bishara ta wurin baiwar alherin Allah da aka yi mini
ta wurin ikonsa da yake aiki a cikina. 8 Ko da yake ni ba kome ba ne a cikin dukan
mutanen Ubangiji, aka ba ni wannan baiwa mai daraja don in faɗa wa Al'ummai
cewa saboda Kiristi akwai albarkun da suka wuce gaban misali. 9 An zaɓe ni in
bayyana wa dukan mutane shirin asirin nan wanda Allah, mahaliccin kome, ya ɓoye
shekara da shekaru. 10 Nufinsa shi ne, yanzu, ta wurin ikkilisiya, a sanar da hikima
iri dabam-dabam na Allah ga masu mulki, da masu iko a samaniya. 11 Wannan shi ne
madawwamin shirinsa, kuma an aikata shi ta wurin Kiristi Yesu Ubangijinmu. 12 A
cikinsa, kuma ta wurin bangaskiya a cikinsa ne muke da ƙarfin halin zuwa kusa da
Allah gabagadi. 13 Don haka, ina roƙonku kada ku fid da zuciya saboda abin da ake
yi mini a nan. Ai, saboda ku ne nake shan wahalolin nan, wannan kuwa ɗaukakarku
ce.

### *Addu'a saboda Afisawa*

14 Saboda wannan ne nake a durƙushe a gaban Uba, 15 wanda ya ba wa kowane
iyali a sama da ƙasa suna. 16 Ina addu'a cewa daga yalwar ɗaukakarsa zai ƙarfafa
ku da iko daga ciki ta wurin Ruhunsa. 17 Ina addu'a domin Kiristi yǎ zauna a cikin
zukatanku ta wurin bangaskiya. Ina kuma addu'a saboda ku da kuka kahu sosai
cikin ƙauna, 18 don ku sami iko, tare da dukan tsarkaka, ku fahimci fāɗi, tsawo, da
kuma zurfin ƙaunar Kiristi take. 19 Ku kuma san wannan ƙauna wadda ta fi gaban
sani, domin a cika ku da dukan cikar Allah.
20 Bari ɗaukaka ta tabbata a gare shi shi wanda yake da ikon yin aiki a cikinmu,
yana kuma aikata abubuwa fiye da dukan abin da muke roƙo, ko muke tunani. 21 Bari
ɗaukaka ta tabbata a gare shi a cikin ikkilisiya da kuma a cikin Kiristi Yesu, har yǎ
zuwa dukan zamanai, har abada abadin! Amin.

# 4

### *Tarayya a cikin jikin Kiristi*

1 A matsayina na ɗan kurkuku saboda Ubangiji, ina roƙonku ku yi rayuwar da ta
dace da kiran da aka yi muku. 2 Kullum ku kasance masu sauƙinkai da kuma hankali;
ku zama masu haƙuri, kuna jimrewa da juna cikin ƙauna. 3 Ku yi ƙoƙari sosai ku
kiyaye zaman ɗayan nan da Ruhu ya ba ku, ku yi haka ta wurin zaman lafiya da
juna. 4 Dukanku jiki ɗaya ne, kuna kuma da Ruhu guda. An ba ku bege guda sa'ad
da aka kira ku. 5 Ubangiji ɗaya, bangaskiya ɗaya, baftisma kuma ɗaya, 6 Allah ɗaya
Uban duka, wanda yake a bisa duka, ta wurin duka, a cikin duka kuma.
7 Amma ga kowannenmu an ba da alheri bisa ga yadda Kiristi ya rarraba. 8 Shi ya
sa aka* ce,
"Sa'ad da ya hau sama,
ya bi da kamammu kamar tawagarsa
ya kuma ba da baye-baye ga mutane."†
9 (Me ake nufin da "ya hau," in ba cewa dā ya sauka can ƙarƙashin ƙasa ba? 10 Shi
wannan da ya sauka ɗin, shi ne kuma ya hau zuwa can sama, kai, gaba da sammai,
don mulkinsa yǎ cika duniya gaba ɗaya.) 11 Saboda haka Kiristi kansa ya ba wa
waɗansu baiwa su zama manzanni, waɗansu su zama annabawa, waɗansu su zama
masu wa'azi, waɗansu kuma su zama fastoci, da kuma malamai. 12 Ya yi haka don

---
* **4:8** Ko kuwa Allah † **4:8** Zab 68.18

yă shirya mutanensa saboda ayyukan hidima, don a gina jikin Kiristi. 13 Wannan zai
ci gaba har sai mun zama ɗaya a cikin bangaskiya da kuma ta wurin fahimtarmu na
Ɗan Allah. Sa'an nan za mu zama balagaggu, kamar yadda Kiristi yake, mu kuma
zama gaba ɗaya cikakku kamar sa.
14 An yi wannan kuwa don kada mu koma zama kamar yara, muna ta canja
zukatanmu game da abin da muka gaskata don kawai wani ya faɗa mana wani abu
dabam, ko domin wani ya yi wayo ya ruɗe mu, ya sa ƙarya ta zama kamar gaskiya.
15 Ya kamata kullum ƙauna tă sa mu faɗa gaskiya. Ta haka za mu yi girma a kowace
hanya, mu kuma zama kamar Kiristi, wanda yake kan 16 dukan jiki. Shi ne ya haɗe
jiki duka, ya kuma sa dukan gaɓoɓin jiki suna aiki daidai, yayinda kowace gaɓa take
aikinta cikin ƙauna.

### *Yin rayuwa kamar 'ya'yan haske*

17 To, ina dai faɗa muku, ina kuma nace faɗa muku a cikin Ubangiji, cewa kada ku
ci gaba da yin rayuwa kamar yadda Al'ummai suke yi, masu banzan tunani. 18 Suna
a cikin duhu a fahimtarsu, kuma a rabe suke daga ran Allah saboda jahilcin da yake
cikinsu ta dalilin taurarewar zukatansu. 19 Ba sa damu da wani abu ko mai kyau ko
marar kyau. Rayukansu sun cika da kowace irin ƙazanta da haɗama.
20 Amma ba abin da aka koya muku ke nan ba sa'ad da kuka zo ga sanin Kiristi.
21 Da yake kun ji duka game da shi, kuka kuma koyi gaskiyar da take cikin Yesu, 22 sai
ku tuɓe tsohon mutumin nan naku da kuma rayuwarku ta dā, wadda take lalacewa
saboda sha'awace-sha'awacen da suke ruɗe ku. 23 A maimakon haka, bari Ruhu yă
sabunta tunaninku da kuma halayenku. 24 Ku sanya sabon halin nan da aka halitta
bisa ga kamannin Allah, halin nan kuwa, yă bayyana cikin adalci, da zaman tsarki.
25 Saboda haka dole kowannenku yă bar yin ƙarya, yă kuma riƙa faɗa wa
maƙwabcinsa gaskiya, gama dukanmu gaɓoɓi jiki ɗaya ne. 26 "Cikin fushinku kada
ku yi zunubi."‡ Kada ku bar rana ta fāɗi kuna fushi, 27 kada kuma ku ba wa Iblis
dama. 28 Duk wanda yake sata, sai yă daina sata, dole kuma yă yi aiki, yă yi wani
abu mai amfani da hannuwansa, don yă sami abin da zai iya raba da masu bukata.
29 Kada wata ƙazamar magana ta fita daga bakunanku, sai dai abin da yake da
amfani don gina waɗansu bisa ga bukatunsu. Ta haka maganarku za tă zama da
amfani ga masu jinta. 30 Kada kuma ku ɓata wa Ruhu Mai Tsarki na Allah rai, wanda
da shi aka hatimce ku da shi don ranar fansa. 31 Ku rabu da kowane irin ɗacin rai,
haushi da hasala, faɗa da ɓata suna, ku rabu da kowace irin ƙeta. 32 Ku yi alheri, ku
kuma ji tausayin juna, kuna gafarta wa juna, kamar yadda a cikin Kiristi, Allah ya
gafarta muku.

## 5

1 Ku zama masu koyi da Allah, kamar ƙaunatattun 'ya'ya, 2 ku kuma yi rayuwar
ƙauna, kamar yadda Kiristi ya ƙaunace mu, har ya ba da kansa dominmu a matsayin
sadaka mai ƙanshi da kuma hadaya ga Allah.
3 Kada a ma ambaci fasikanci, da kowane irin aikin lalata, ko kwaɗayi a tsakaninku,
domin bai dace da mutane masu tsarki na Allah ba. 4 Haka ma bai kamata a sami
datti, ƙazamar magana, ko zancen banza a cikinku ba, domin ba su dace ba, a
maimakon haka sai ku yi ta yin godiya. 5 Ku dai tabbata, ba wani mai fasikanci,
ko mai aikin lalata, ko mai kwaɗayin (wanda shi da mai bautar gumaka ɗaya ne), da
yake da gādo a mulkin Kiristi da na Allah. 6 Kada wani yă ruɗe ku da kalmomin wofi,
gama saboda waɗannan abubuwa ne fushin Allah yake zuwa a kan marasa biyayya.
7 Saboda haka kada ku haɗa kai da su.

‡ **4:26** Zab 4.4

8 Gama a dā zukatanku sun cika da duhu, amma yanzu ku haske ne a cikin Ubangiji.
Ku yi rayuwa kamar ʼyaʼyan haske 9 (domin amfanin haske ya ƙunshi nagarta, adalci,
da kuma gaskiya) 10 ku nemi abin da zai gamshi Ubangiji. 11 Ku yi nesa da ayyukan
duhun da mutane suke yi, a maimakon haka, ku tona su. 12 Gama abin kunya ne a ma
faɗi abubuwan da marasa biyayya suke yi a ɓoye. 13 Duk abin da aka kawo a gaban
haske ana iya ganinsa, kuma duk abin da aka haskaka yakan zama haske. 14 Shi ya
sa aka ce,

"Ka farka, ya kai mai barci,
ka tashi daga matattu,
Kiristi kuwa zai haskaka ka."

15 Sai ku yi hankali sosai da yadda kuke rayuwa, kada ku zama kamar marasa
hikima, sai dai kamar masu hikima. 16 Ku kuma yi matuƙar amfani da kowane zarafi,
don kwanakin nan mugaye ne. 17 Saboda haka kada ku zama wawaye, sai dai ku
fahimci ko mene ne nufin Ubangiji. 18 Kada ku bugu da ruwan inabi, wanda yake
kai ga lalaci. A maimako haka, ku cika da Ruhu. 19 Ku yi zance da juna cikin zabura,
da waƙoƙi, da kuma waƙoƙin ruhaniya. Ku rera, ku kuma yi kiɗe-kiɗe a zuciyarku
ga Ubangiji. 20 Kullum ku dinga yin amfani da sunan Ubangijinmu Yesu Kiristi, kuna
gode wa Allah Uba a kome.

### *Mata da maza*

21 Ku yi biyayya da juna saboda bangirmar da kuke nuna wa Kiristi.

22 Matan aure, ku yi biyayya ga mazanku, kamar ga Ubangiji ne kuke yi. 23 Gama
miji shi ne kan mace, yadda Kiristi yake kai da kuma Mai Ceton ikkilisiya, wadda
take jikinsa. 24 To, kamar yadda ikkilisiya take biyayya ga Kiristi, haka ma ya kamata
mata su yi biyayya ga mazansu cikin kome.

25 Maza, ku ƙaunaci matanku, kamar yadda Kiristi ya ƙaunaci ikkilisiya, ya kuma
ba da kansa dominta. 26 Ya mai da ikkilisiya ta zama mai tsarki ta wurin ikon
maganarsa, ya kuma tsabtacce ta ta wurin wanke ta da ruwa. 27 Kiristi ya yi haka
don yǎ miƙa wa kansa ikkilisiya mai ɗaukaka da kuma mai tsarki, marar aibi, marar
tabo, da kuma marar lahani. 28 Don haka, dole maza su ƙaunaci matansu kamar
yadda suke ƙaunar jikunansu. Wanda yake ƙaunar matarsa, yana ƙaunar kansa ne.
29 Gama ba wanda ya taɓa ƙin jikinsa, sai dai yǎ ciyar da shi, yǎ kuma kula da shi,
kamar yadda Kiristi yake yi wa ikkilisiya, 30 gama mu gaɓoɓin jikinsa ne. 31 "Saboda
haka mutum yakan bar mahaifinsa da mahaifiyarsa, yǎ manne wa matarsa, su biyun
su zama jiki ɗaya."* 32 Wannan babban asiri ne, amma na ɗauke shi a matsayin
kwatanci ne na Kiristi da ikkilisiya. 33 Duk da haka, dole kowannenku yǎ ƙaunaci
matarsa kamar yadda yake ƙaunar kansa, kuma dole matar tǎ yi biyayya ga mijinta.

# 6

### *ʼYaʼya da iyaye*

1 Ku ʼyaʼya, ku yi biyayya ga iyayenku, gama ku na Ubangiji, abin da ya dace ku yi
ke nan. 2 Doka ta farko wadda aka haɗa da alkawari ita ce, "Ka girmama mahaifinka
da mahaifiyarka, 3 don ka zauna lafiya, ka kuma yi tsawon rai a duniya."*

4 Ku kuma iyaye, kada ku tsokane ʼyaʼyanku. Ku yi musu reno mai kyau. Ku koyar
da su, ku kuma gargaɗe su game da Ubangiji.

### *Bayi da iyayengiji*

5 Ku bayi, ku yi biyayya ga iyayengijinku na duniya. Ku nuna musu halin bangirma,
kuna kuma yin musu biyayya cikin dukan abu, da zuciya ɗaya kamar ga Kiristi kuke
yi. 6 Ku yi aiki sosai, ba don kawai ku gamshe su saʼad da suke kallonku ba. Da

* **5:31** Far 2.24 * **6:3** M Sh 5.16

yake ku bayin Kiristi ne, ku aikata nufin Allah da dukan zuciyarku. 7 Ku yi aikinku
da kyakkyawar niyya, sai ka ce ga Ubangiji kuke yi, ba mutane ba. 8 Gama kun san
cewa Ubangiji zai ba da lada ga kowa gwargwadon kowane aiki nagarin da ya yi, ko
shi bawa ne, ko ʼyantacce.
9 Ku kuma masu bayi, dole ku bi da bayinku da kyau. Ku daina ba su tsoro. Ku
tuna, ku da su, Maigida ɗaya kuke da shi a sama, kuma ba ya nuna bambanci.

### *Kayan yaƙi na Allah*

10 A ƙarshe, bari ƙarfin ikon Ubangiji yǎ ba ku ƙarfi. 11 Ku yafa dukan kayan yaƙin
da Allah yake bayarwa, don ku iya kāre kanku daga dabarun Shaiɗan. 12 Gama ba da
mutane da suke nama da jini ne muke yaƙi ba. Muna yaƙi ne da ikoki, da hukumomi,
da masu mulkin duhu, da kuma a ikokin da suke cikin a sararin sama. 13 Saboda haka
sai ku yafa dukan kayan yaƙi na Allah, domin saʼad da ranar mugun nan ta zo, ku iya
yin tsayin daka, bayan kuma kuka gama kome, ku dāge. 14 Saboda haka fa ku dāge,
ku sa gaskiya tǎ zama ɗamararku, adalci yǎ zama sulkenku, 15 shirin kai bisharar
salama yǎ zama kamar takalmi a ƙafafunku. 16 Ban da waɗannan kuma, ku ɗauki
garkuwar bangaskiya, wadda za ku iya kashe dukan kibiyoyin wutar Mugun nan da
ita. 17 Ku kuma ɗauki hular kwano na ceto, da takobin Ruhu, wato, Maganar Allah.
18 A koyaushe ku kasance kuna adduʼa da roƙo ta wurin ikon Ruhu ba fasawa. A kan
wannan manufa ku zauna a faɗake da matuƙar naci, kuna yin wa dukan mutanen
Ubangiji adduʼa. 19 Ku kuma yi adduʼa domina, don duk saʼad da na buɗe bakina, in
sami kalmomi babu tsoro, don in sanar da asirin bishara, 20 wadda nake jakadanta
cikin sarƙoƙi. Ku yi adduʼa don in iya yin shelarta babu tsoro, yadda ya kamata in
yi.

### *Gaisuwar ƙarshe*

21 Tikikus, ƙaunataccen ɗanʼuwa da kuma amintaccen bawa cikin Ubangiji, zai
faɗa muku kome, domin ku ma ku san yadda nake, da kuma abin da nake yi. 22 Na
aike shi gare ku musamman don wannan, domin ku san yadda muke, yǎ kuma
ƙarfafa ku.

23 ʼYanʼuwa, salama tare da ƙauna da kuma bangaskiya daga Allah Uba da Ubangiji
Yesu Kiristi su kasance tare da ku.

24 Alheri yǎ tabbata ga dukan masu ƙaunar Ubangiji Yesu Kiristi da ƙauna marar
ƙarewa.

# Filibbiyawa

1 Bulus da Timoti, bayin Kiristi Yesu,

Zuwa ga dukan tsarkaka cikin Kiristi Yesu a Filibbi, tare da masu kula da Ikkilisiya*
da kuma masu hidima.

2 Alheri da salama daga Allah Ubanmu da kuma Ubangiji Yesu Kiristi, su kasance
tare ku.

## *Godiya da addu'a*

3 Ina gode wa Allahna a kowane lokacin da na tuna da ku. 4 A cikin dukan
addu'o'ina dominku duka, nakan yi addu'a da farin ciki kullum 5 saboda tarayyarku
a cikin bishara daga ranar farko har yă zuwa yanzu, 6 da tabbacin cewa wanda ya
fara kyakkyawan aikin nan a cikinku, zai kai shi ga kammalawa har yă zuwa ranar
Kiristi Yesu.
7 Daidai ne in yi wannan tunani game da dukanku, da yake kuna a zuciyata; domin
ko ina daure cikin sarƙoƙi ko ina kāre bishara ina kuma tabbatar da ita, dukanku
kuna tarayya cikin alherin Allah tare da ni. 8 Allah shi ne shaidata, ya san yadda
nake ƙaunarku duka da ƙaunar Kiristi Yesu.
9 Addu'ata ita ce ƙaunarku tă yi ta cin gaba da ƙaruwa cikin sani da kuma zurfin
ganewa, 10 don ku iya rarrabe abin da yake mafi kyau, ku kuma zama da tsarki,
marasa aibi har yă zuwa ranar Kiristi, 11 cikakku da sakamakon aikin adalci da yake
zuwa ta wurin Yesu Kiristi, zuwa ga ɗaukakar Allah da kuma yabonsa.

## *Sarƙoƙin Bulus sun sa ci gaban bishara*

12 To, ina so ku sani 'yan'uwa, cewa abin da ya faru da ni ya sa cin gaban bishara.
13 Ta haka, ya zama sananne ga dukan masu gadin fada† da kuma ga kowa cewa an
daure ni da sarƙoƙi saboda Kiristi. 14 Saboda sarƙoƙina, yawancin 'yan'uwa cikin
Ubangiji sun sami ƙarfafawa su yi maganar Allah gabagadi da kuma babu tsoro.
15 Gaskiya ce cewa waɗansu suna yin wa'azin Kiristi saboda kishi da neman faɗa,
amma waɗansu da nufi mai kyau suke yi. 16 Na biye suna yin haka cikin ƙauna, da
sanin cewa an sa ni a nan ne domin kāriyar bishara. 17 Na farin dai suna wa'azin
Kiristi da sonkai ne, ba da zuciya ɗaya ba, a sonsu, su wahalar da ni a cikin sarƙoƙi.‡
18 Me kuma? Ta ko yaya dai, ko da gangan, ko da gaske, ana shelar Kiristi. Domin
wannan kuwa ina farin ciki.
I, zan kuwa ci gaba da farin ciki, 19 gama na san cewa ta wurin addu'o'inku da kuma
taimako daga Ruhun Yesu Kiristi, abin da ya same ni zai zama sanadin kuɓutata.
20 Ina saurara da marmari da kuma bege cewa ba zan taɓa shan kunya ba, sai dai
zan sami issashen ƙarfin hali yanzu kamar kullum, za a ɗaukaka Kiristi a jikina, ko ta
wurin rayuwa ko kuma ta wurin mutuwa. 21 Gama a gare ni, rai Kiristi ne, mutuwa
kuma riba ce. 22 In zan ci gaba da rayuwa a cikin jiki, wannan zai zama aiki mai
amfani a gare ni. Duk da haka me zan zaɓa? Ban sani ba! 23 Na rasa wanda zan zaɓa
cikin biyun nan. Ina sha'awa in yi ƙaura in zauna tare da Kiristi, wannan kuwa ya
fi kyau nesa ba kusa ba; 24 amma ya fi muku muhimmanci in rayu cikin jiki. 25 Na
tabbata haka ne, na kuwa san zan wanzu in zauna tare da ku duka, domin ku ci gaba,

---

* **1:1** A al'adance su bishob † **1:13** Ko kuwa dukan fada ‡ **1:17** Waɗansu rubuce-rubucen hannun da ba su daɗe ba suna da aya 17 kafin aya 16.

bangaskiyarku tana sa ku farin ciki, 26 domin ta wurin kasancewata tare da ku, farin
cikinku cikin Kiristi Yesu zai cika sosai ta dalilina.

### *Rayuwar da ta dace da bishara*

27 Kome ya faru, ku yi zaman da ya cancanci bisharar Kiristi. Ta haka, ko na zo na
gan ku, ko ban zo ba, in ji labari cewa kun tsaya da ƙarfi a cikin ruhu ɗaya, kuna
fama kamar mutum ɗaya saboda bangaskiyar bishara 28 ba tare da kun ji tsoron
waɗanda suke gāba da ku ta kowace hanya ba. Wannan alama ce a gare su cewa za
a hallaka su, amma a gare ku za a cece ku, wannan tabbacin kuwa daga wurin Allah
ne. 29 Gama an ba ku zarafi a madadin Kiristi cewa ba gaskatawa da shi kaɗai ba
kuka yi ba, har ma ku sha wahala dominsa, 30 da yake kuna shan faman da kuka gan
na sha, kuna kuma jin cewa har yanzu ina sha.

# 2

### *Koyi tawali'un Kiristi*

1 In kuna da wata ƙarfafawa daga tarayya da Kiristi, in da wata ta'aziyya daga
ƙaunarsa, in da wani zumunci da Ruhu, in da juyayi da tausayi, 2 to, sai ku sa farin
cikina yă zama cikakke ta wurin kasance da hali ɗaya, kuna ƙauna ɗaya, kuna zama
ɗaya cikin ruhu da kuma manufa. 3 Kada ku yi kome da sonkai ko girman kai, sai
dai cikin tawali'u, ku ɗauki waɗansu sun fi ku. 4 Bai kamata kowannenku yă kula
da sha'anin kansa kawai ba, sai dai yă kula da sha'anin waɗansu ma.

5 A cikin dangantakarku da juna, ya kamata halayenku su zama kamar na Kiristi
Yesu.

6 Wanda, ko da yake cikin ainihin surar Allah yake,
bai mai da daidaitakansa nan da Allah wani abin riƙewa kam-kam ba,
7 amma ya mai da kansa ba kome ba,
yana ɗaukan ainihin surar bawa,
aka yi shi cikin siffar mutum.
8 Aka kuma same shi a kamannin mutum,
ya ƙasƙantar da kansa
ya kuma zama mai biyayya wadda ta kai shi har mutuwa,
mutuwar ma ta gicciye!

9 Saboda haka Allah ya ɗaukaka shi zuwa mafificin wuri
ya kuma ba shi sunan da ya fi dukan sunaye,
10 don a sunan Yesu kowace gwiwa za tă durƙusa,
a sama da a ƙasa da kuma a ƙarƙashin ƙasa,
11 kowane harshe kuma yă furta cewa Yesu Kiristi Ubangiji ne,
don ɗaukakar Allah Uba.

### *Haskaka kamar taurari*

12 Saboda haka, ya abokaina ƙaunatattu, kamar yadda kullum kuke biyayya ba
kawai sa'ad da ina nan ba, amma yanzu da ba na nan tare da ku, ku ci gaba da yin
ayyukan cetonku da tsoro da kuma rawan jiki, 13 gama Allah ne yake aiki a cikinku,
don ku nufa ku kuma aikata bisa ga nufinsa mai kyau.

14 Ku yi kome ba tare da gunaguni ko gardama ba, 15 don ku zama marasa abin
zargi, sahihai 'ya'yan Allah, waɗanda ba su da laifi, a zamanin mutane karkatattu,
kangararru, waɗanda kuke haskakawa a cikinsu kamar fitilu a duniya 16 kuna kuwa
cin gaba da riƙe maganar rai domin in yi taƙama a ranar Kiristi cewa ban yi gudu
ko fama a banza ba. 17 Amma ko da ana tsiyaye jinina kamar hadaya ta sha a kan
hadaya da kuma hidimar da take fitowa daga bangaskiyarku, ina murna ina kuma

farin ciki da ku duka. 18 Haka ma ya kamata ku yi murna ku kuma yi farin ciki tare
da ni.

### *Timoti da Afaforiditus*

19 Ina sa rai a cikin Ubangiji Yesu cewa zan aika da Timoti zuwa gare ku ba da
daɗewa ba, don ni ma in ji daɗi sa'ad da na ji labarinku. 20 Ba ni da wani kamar
sa, wanda yake da ainihin sha'awa a zaman lafiyarku. 21 Gama kowa yana lura da
al'amuran kansa ne kawai, ba na Kiristi Yesu ba. 22 Amma, ai, kun san darajar Timoti
yadda muka yi bautar bishara tare, kamar ɗa da mahaifinsa. 23 Saboda haka, ina sa
rai, in aike shi da zarar na ga yadda abubuwa suke a nan. 24 Ni kuma ina da tabbaci
a cikin Ubangiji cewa zan zo ba da daɗewa ba.
25 Amma ina gani ya dace in aika da Afaforiditus, ɗan'uwana, abokin aikina da
kuma abokin famana, wanda kuma yake ɗan saƙonku, wanda kuka aika domin yă
biya mini bukatuna. 26 Gama yana marmarin ganinku duka ya kuma damu domin
kun ji cewa ya yi rashin lafiya. 27 Ba shakka ya yi rashin lafiya, har ya kusa mutuwa.
Amma Allah ya nuna masa jinƙai, ba shi kaɗai ba amma har da ni ma, don yă rage
mini baƙin ciki kan baƙin ciki. 28 Saboda haka na yi niyya ƙwarai in aike shi wurinku,
don sa'ad da kuka sāke ganinsa za ku yi murna, ni kuma in rage damuwa. 29 Ku
marabce shi cikin Ubangiji da farin ciki mai yawa, ku kuma girmama mutane irinsa,
30 domin ya kusa yă mutu saboda aikin Kiristi, ya yi kasai da ransa don yă cikasa
taimakon da ba ku iya yi mini ba.

# 3

### *Ban da dogara a jiki*

1 A ƙarshe, 'yan'uwana, ku yi farin ciki a cikin Ubangiji! Ba abin damuwa ba ne a
gare ni in sāke rubuta muku irin waɗannan abubuwa, domin lafiyarku ne. 2 Ku yi
hankali da waɗancan karnuka, waɗancan mutane masu aikata mugunta, waɗancan
masu yankan jiki. 3 Gama mu ne masu kaciya, mu da muke yi sujada ta wurin Ruhun
Allah, mu da muke taƙama a cikin Kiristi Yesu, mu da ba mu dogara da ayyukan da
ake gani ba, 4 ko da yake ni kaina ina da dalilan dogara da haka.
In kuwa akwai wani wanda yake tsammani yana da dalilan dogara ga jiki, ni fa na
fi shi, 5 an yi mini kaciya a rana ta takwas, asalina Isra'ila ne, na kabilar Benyamin,
mutumin Ibraniyawa ɗan Ibraniyawa; bisa ga doka kuwa ni Bafarisiye ne; 6 wajen
himma kuwa, ni mai tsananta wa ikkilisiya ne, wajen aikin adalci bisa ga hanyar
doka, ni marar laifi ne.
7 Amma abin da dā ya zama mini riba yanzu, na ɗauka hasara ce saboda Kiristi.
8 Me kuma ya fi, na ɗauki dukan abubuwa hasara ne in aka kwatanta da mafificiyar
girman sanin Kiristi Yesu Ubangijina, wanda saboda shi ne na yi hasarar kome. Na
mai da su kayan wofi, domin in sami Kiristi 9 a kuma same ni a cikinsa, ba da wani
adalcin kaina wanda yake zuwa daga bin doka ba, sai dai adalcin da yake samuwa
ta wurin bangaskiya a cikin Kiristi, adalcin da yake fitowa daga Allah da kuma yake
zuwa ta wurin bangaskiya. 10 Ina so in san Kiristi da ikon tashinsa daga matattu
da kuma zumuncin tarayya cikin shan wahalarsa, in kuma zama kamar sa a cikin
mutuwarsa, 11 yadda kuma ko ta yaya, in kai ga tashin nan daga matattu.
12 Ba cewa na riga na sami dukan wannan ba ne, ko kuma an riga an mai da ni
cikakke ba, sai dai ina nacewa don in kai ga samun abin da Kiristi Yesu ya riƙe ni
saboda shi. 13 'Yan'uwa, ban ɗauki kaina a kan cewa na riga na sami abin ba. Sai
dai abu guda nake yi. Ina mantawa da abin da yake baya, ina kuma nacewa zuwa ga
samun abin da yake gaba, 14 ina nacewa gaba zuwa ga manufar, don in sami ladar
da Allah ya yi mini na kiran nan zuwa sama a cikin Kiristi Yesu.

*Nacewa zuwa ga manufar*
15 Dukanmu da muka balaga ya kamata mu yi wannan irin ganin abubuwa. In
kuwa saboda wani dalili tunaninku ya yi dabam, Allah zai bayyana muku wannan
ma. 16 Sai dai a duk inda muka kai, mu ci gaba da haka.
17 Ku haɗa kai da waɗansu cikin bin gurbina, ku kuma lura da waɗanda suke
rayuwa bisa ga ƙa'idar da muka ba ku. 18 Gama kamar yadda na sha gaya muku
yanzu kuma ina sāke gaya muku har ma da hawaye, waɗansu da yawa suna rayuwa
kamar abokan gāban gicciyen Kiristi. 19 Kaddararsu hallaka ce, allahnsu cikinsu
ne, rashin kunyarsu shi ne abin fahariyarsu. Hankalinsu yana kan kayan duniya.
20 Amma mu 'yan mulkin sama ne. Muna kuma jira zuwan Mai Ceto daga can,
Ubangiji Yesu Kiristi, 21 shi ne mai ikon kawo dukan abubuwa ƙarƙashin mulkinsa.
Ta wurin ikon nan nasa zai sāke jikin nan namu na ƙasƙanci, yǎ mai da shi kamar
jikin nan nasa na ɗaukaka.

## 4

1 Saboda haka 'yan'uwana, ku da nake ƙauna, nake kuma marmarin ganinku, ku
da kuke farin cikina da kuma rawanina, ku dāge ga Ubangiji, ya ku ƙaunatattuna!
2 Ina roƙon Yuwodiya ina kuma roƙon Sintike, su yi zaman lafiya da juna saboda
su na Ubangiji ne. 3 I, ina kuma roƙonka, abokin famata, ka taimaki matan nan
waɗanda suka yi fama aikin bishara tare da ni, haka ma Kilemen da kuma sauran
abokan aikina, waɗanda sunayensu suna cikin littafin rai.

*Gargaɗi*
4 Ku yi farin ciki a cikin Ubangiji kullum. Ina sāke gaya muku ku yi farin ciki! 5 Bari
kowa yǎ kasance da sauƙinkai. Ubangiji ya yi kusan zuwa. 6 Kada ku damu game da
kome sai dai a cikin abu duka, ku gabatar da roƙe-roƙenku ga Allah ta wurin addu'a
da roƙo, tare da godiya. 7 Salamar Allah, wadda ta wuce dukan fahimta, za tǎ tsai da
zukatanku da tunaninku cikin Kiristi Yesu.
8 A ƙarshe, 'yan'uwa, duk abin da yake na gaskiya, duk abin da yake na
girmamawa, duk abin da yake daidai, duk abin da yake da tsarki, duk abin da yake
kyakkyawa, duk abin da yake na sha'awa, in ma wani abu mafifici ne, ko ya cancanci
yabo, ku yi tunani a kan irin abubuwan nan. 9 Duk abin da kuka koya ko kuka karɓa
ko kuka ji daga wurina, ko kuka gani a cikina, ku yi aiki da shi. Allah na salama
kuma zai kasance tare da ku.

*Godiya saboda kyautansu*
10 Na yi farin ciki sosai ga Ubangiji don yanzu kun sāke nuna kun kula da ni. Ko
da yake dā ma kun kula da ni sai dai ba ku sami dama ku nuna mini ba. 11 Ba na
faɗin haka domin ina cikin bukata, gama na koya yadda zan gamsu a cikin kowane
hali. 12 Na san mene ne zaman rashi, na kuma san mene ne zaman samu. Zan iya
zama cikin kowane hali, ko cikin ƙoshi ko cikin yunwa, ko cikin yalwa ko kuma cikin
fatara. 13 Ina iya yin kome ta wurin wannan wanda yake ba ni ƙarfi.
14 Duk da haka kun kyauta da kuka yi tarayya da ni cikin wahalolina. 15 Ban da
haka, kamar yadda ku Filibbiyawa kuka sani, a farkon kwanakin da kuka ji bishara,
sa'ad da na tashi daga Makidoniya, babu wata ikkilisiyar da tǎ yi tarayya da ni a
fannin bayarwa da karɓa, sai ku kaɗai; 16 gama ko sa'ad da nake a Tessalonika ma,
kun aiko mini da taimako sau da sau sa'ad da nake cikin bukata. 17 Ba cewa ina
neman kyauta ba ne, sai dai ina neman abin da za a ƙara a kan ribarku. 18 An biya
ni duka, biyan da ya wuce misali. Bukatata ta biya, da yake na karɓi kyautarku da
kuka aiko ta hannun Afaforiditus. Baiwa mai ƙanshi, hadaya abar karɓa, mai faranta
wa Allah rai. 19 Allahna kuma zai biya dukan bukatunku bisa ga ɗaukakar wadatarsa
cikin Kiristi Yesu.

20 Ɗaukaka ta tabbata ga Allahnmu da Ubanmu har abada abadin. Amin.

### *Gaisuwa ta ƙarshe*

21 Ku gai da dukan tsarkaka cikin Kiristi Yesu.
'Yan'uwan da suke tare da ni suna gaishe ku.
22 Dukan tsarkaka suna gaishe ku, musamman waɗanda suke na gidan Kaisar.

23 Alherin Ubangiji Yesu Kiristi yă kasance da ruhunku. Amin.*

* **4:23** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā ba su da Amin.

# Kolossiyawa

1 Bulus, wanda Allah ya zaɓa don yă zama manzon Kiristi Yesu, da kuma daga
Timoti ɗan'uwanmu,

2 Zuwa ga tsarkaka da kuma amintattun 'yan'uwa cikin Kiristi da suke a Kolossi.

Alheri da salama daga Allah Ubanmu, su kasance tare da ku.*

### *Godiya da addu'a*

3 Kullum muna gode wa Allah, Uban Ubangijinmu Yesu Kiristi, sa'ad da muke
addu'a dominku. 4 Gama mun ji labarin bangaskiyarku a cikin Yesu Kiristi da kuma
ƙaunar da kuke yi saboda dukan tsarkaka. 5 Kuna yin haka ne kuwa domin abin
da kuke bege yana a ajiye a sama. Kun riga kun ji game da wannan bege sa'ad da
kuka gaskata saƙon nan na gaskiya wanda shi ne bisharar 6 da ta zo muku. Ko'ina
a duniya wannan bishara tana yi ta haihuwa tana kuma girma, kamar yadda take yi
a cikinku tun daga ranar da kuka ji ta kuka kuma fahimci alherin Allah cikin dukan
gaskiyarta. 7 Kun koyi wannan gaskiya daga wurin Efafaras, ƙaunataccen abokin
hidimarmu, wanda yake amintacce mai hidimar Kiristi a madadinmu, 8 wanda kuma
ya faɗa mana ƙaunar da kuke yi cikin Ruhu.
9 Shi ya sa tun daga ranar da muka sami labarin, ba mu fasa yin addu'a dominku ba.
Kullum muna roƙon Allah yă sa ku san kome da yake so ku yi, domin ku sami hikima
ta Ruhu, ku kuma sami ganewar kome duka. 10 Ta haka za ku yi rayuwa wadda ta
dace da Ubangiji, ku kuma gamshe shi a ta kowace hanya, kuna yin aiki mai kyau
ta kowace hanya, kuna kuma yin girma cikin sanin Allah. 11 Allah yă ƙarfafa ku da
dukan iko bisa ga ɗaukakar ƙarfinsa domin ku kasance da jimrewa sosai da kuma
haƙuri, cikin farin ciki 12 kuna gode wa Uba, wanda ya sa kuka cancanci ku sami rabo
a gādon tsarkaka a cikin mulkin haske. 13 Gama ya riga ya cece mu daga mulkin duhu
ya kuma kawo mu cikin mulkin Ɗan da yake ƙauna, 14 wanda ta wurinsa muka sami
fansa da kuma gafarar zunubai.

### *Fifikon Kiristi*

15 Kiristi shi ne surar da ake gani na Allah wanda ba a iya gani, ɗan fari a kan
dukan halitta. 16 Ta wurinsa aka halicci dukan abu, abubuwan da suke cikin sama da
abubuwan da suke a duniya, waɗanda ake gani, da waɗanda ba a gani, ko kursiyoyi
ko ikoki ko masu mulki ko hukumomi; an halicci dukan abu ta wurinsa da kuma
dominsa ne. 17 Ya kasance kafin dukan abu, kuma a cikinsa ne dukan abubuwa
suke a harhaɗe. 18 Shi ne kuma kan ikkilisiya, wadda take jikinsa. Shi ne mafari da
kuma na farko da ya tashi daga matattu, domin a cikin kowane abu yă zama mafifici.
19 Gama Allah ya ji daɗi yă sa dukan cikarsa ta kasance a cikin Kiristi, 20 ta wurin
Kiristi ne ya komar da kome zuwa ga kansa. Ya kawo salama ga abubuwan da suke
ƙasa da abubuwan da suke sama, ta wurin jinin Kiristi da ya zubar a kan gicciye.
21 A dā kuna a ware da Allah, kuka kuma zama abokan gāba a cikin tunaninku
saboda mugun halinku. 22 Amma Ɗansa ya zama mutum ya kuma mutu. Saboda
haka Allah ya yi sulhu da ku, yanzu kuwa ya bar ku ku tsaya a gabansa da tsarki,
marasa aibi, da kuma marasa abin zargi. 23 Sai ku ci gaba cikin bangaskiyarku, kuna
tsaye a kafe kuma tsayayyu, ba tare da gusawa daga begen da kuka ji daga bishara

* **1:2** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da Uba da Ubangiji Yesu Kiristi

ba. Wannan ita ce bisharar da kuka ji wadda aka yi shelarta ga kowace halittar da
take ƙarƙashin sama, wadda kuma ni Bulus, na zama mai hidimarta.

*Hidimar Bulus ga ikkilisiya*

24 Yanzu, ina farin ciki saboda wuyar da nake sha dominku, don ta wurin wuyan
nan zan cika abin da ya rage na wuyar da Kiristi ya sha saboda jikinsa, wato,
ikkilisiya. 25 Na zama mai hidimar ikkilisiya bisa ga aikin nan da Allah ya ba ni
amana saboda ku, domin in sanar da maganar Allah sosai. 26 Wannan magana da
nake gaya muku asiri ne da yake a ɓoye tun zamanai masu yawa, wanda yanzu aka
bayyana ga tsarkaka. 27 Su ne Allah ya so yǎ sanar da yadda irin yalwar ɗaukakar
asirin nan take a cikin al'ummai, asirin nan kuwa shi ne Kiristi a cikinku, begen
ɗaukakar da za a bayyana.
28 Saboda haka ko'ina muka tafi, muna shela, muna gargaɗi, muna kuma koyar da
kowa da dukan hikima, don mu miƙa kowa cikakke a cikin Kiristi. 29 Don haka ne
ina fama, ina kuma ƙoƙari da duk ƙarfin nan da Kiristi ya ba ni.

## 2

1 Ina so ku san irin famar da nake yi saboda ku da kuma waɗanda suke a
Lawodiseya, da kuma saboda dukan waɗanda ba su taɓa ganina ido da ido ba.
2 Manufata ita ce a ƙarfafa su su kuma zama ɗaya a cikin ƙauna. Ina so su kasance
da cikakken ƙarfin hali domin suna da cikakken fahimtar asirin Allah, wato, Kiristi
kansa, 3 a cikinsa ne aka ɓoye dukkan dukiya ta hikima da ta sani. 4 Ina faɗa muku
wannan ne don kada wani yǎ ruɗe ku da daɗin baki. 5 Gama ko da yake ba na nan
tare da ku a cikin jiki, ina tunaninku kullum, ina kuma farin ciki da gani kuna rayuwa
yadda ya kamata, kuna kuma dāgewarku a kan bangaskiyarku a cikin Kiristi.

*'Yanci daga ƙa'idodin mutane ta wurin rayuwa tare da Kiristi*

6 To, da yake kun karɓi Kiristi Yesu a matsayin Ubangiji, sai ku ci gaba da rayuwa
a cikinsa, 7 ku tsaya daram ku kuma ginu a cikinsa, ku sami ƙarfafawa a cikin
bangaskiya kamar yadda aka koya muku, kuna kuma cike da godiya.
8 Ku lura kada wani yǎ ruɗe ku da ilimin banza da wofi. Wannan koyarwa ta
mutane ce kawai. Ta fito daga ikokin wannan duniya ne* ba daga Kiristi ba.
9 Gama a cikin Kiristi cikin jiki dukkan cikar Allahntaka take tabbata, 10 an kuma
mai da ku cikakku a cikin Kiristi, wanda yake shi ne kai a kan kowane iko da kuma
hukuma. 11 A cikinsa ne kuma aka yi muku kaciya, ba kuwa yin mutum ba, amma
wadda Kiristi ya yi muku, ta wurin tuɓe halinku na mutuntaka. 12 Da yake an
binne ku tare da shi cikin baftisma haka kuma aka tashe ku tare da shi ta wurin
bangaskiyarku a cikin ikon Allah, wanda ya tashe shi daga matattu.
13 Kun zama matattu saboda ku masu zunubi ne kuma saboda halin zunubanku
aka ware. Sa'an nan Allah ya sa kuka rayu tare da Kiristi. Ya gafarta mana dukan
zunubanmu. 14 Ya soke rubutacciyar doka tare da ƙa'idodinta, wadda take gāba
da mu, take kuma hamayya da mu; ya kuma kawar da ta, ya kafe ta a kan gicciye.
15 Bayan ya ƙwace makaman ikoki da hukumomi, ya kunyata su a sarari, ya ci nasara
a bisansu ta wurin gicciye.
16 Saboda haka kada ku bar wani yǎ shari'anta ku a kan abin da kuke ci ko sha, ko
bisa ga abin da ya shafi wani bikin addini, ko Bikin Sabon Wata ko na ranar Asabbaci.
17 Waɗannan su ne hoton abubuwan da za su zo; amma Kiristi ne ainihinsu. 18 Kada
ku yarda wani yǎ ɓata ku, cewa shi wani abu ne don yǎ ga wahayi. Irin mutumin nan
yakan nuna ƙasƙancin kai na ƙarya, yǎ kuma ce yana yi wa mala'iku sujada. Irin

* **2:8** ikokin wannan duniya ne, An ɗauka Ruhohi da ikokin da ba a gani su suke bi da rayuwar mutane sun kuma gaskata sun haɗa da motsin taurari.

mutumin nan yana kumbura kansa ba dalili, sai son zuciya irin na halin mutuntaka.
19 Ya yanke dangantaka da Kiristi wanda yake kai, wanda ta gare shi ne dukan jiki yake a haɗe, yake tsaye ta wurin taimakon gaɓoɓi da jijiyoyi, yana kuma girma kamar yadda Allah yake sa yă yi girma.

20 Kun mutu tare da Kiristi. Yanzu ƙa'idodin wannan duniya ba su da iko a kanku. Don me kuke zama har yanzu kamar ku nasu ne? Kuna biyayya da umarnansu cewa,
21 "Kada ka kama! Kada ka ɗanɗana! Kada ka taɓa"? 22 Irin waɗannan dokoki suna magana a kan abubuwan da ba sa daɗewa. Su ayyukan mutane ne, sun kuma fito daga koyarwar mutane. 23 Yin biyayya da irin waɗannan ƙa'idodi za su yi kamar su ne abu mafi kyau da za a yi. Sukan yi kamar suna sa a ƙaunaci Allah sosai a kuma kasance da sauƙinkai a kuma kasance da kamunkai. Amma ba su da wani iko a kan sha'awace-sha'awacenmu.

# 3

*Umarnai don zaman tsarki*

1 Da yake an tashe ku tare da Kiristi, sai ku sa zukatanku a kan abubuwan da suke sama, inda Kiristi yake zaune a hannun dama na Allah. 2 Ku sa hankulanku a kan abubuwan sama, ba kan abubuwan duniya ba. 3 Gama kun mutu, ranku yanzu kuwa yana ɓoye tare da Kiristi a cikin Allah. 4 Sa'ad da Kiristi, wanda shi ne ranku,* ya bayyana, ku ma za ku bayyana tare da shi cikin ɗaukaka.

5 Saboda haka, sai ku fid da duk wani abin da yake kawo sha'awa a zukatanku, fasikanci, ƙazanta, sha'awa, muguwar sha'awa, da kuma kwaɗayi wanda shi ma bautar gumaka ne. 6 Gama fushin Allah zai sauko a kan masu aikata waɗannan.†
7 Dā kun yi waɗannan abubuwa, sa'ad da rayuwar tana cikin duniya mai wannan hali. 8 Amma yanzu dole ku raba kanku da dukan ire-iren abubuwan nan. Ku daina fushi, ku daina ƙiyayya da ƙeta. Ku bar ɓatan suna da kuma ƙazamar magana daga leɓunanku. 9 Kada ku yi wa juna ƙarya, da yake kun tuɓe tsohon halinku tare da ayyukansa 10 kun ɗauki sabon halin nan da ake sabuntawa ga sani, bisa ga kamannin Mahaliccinsa. 11 A wannan sabuwar rayuwa babu bambanci ko kai mutumin Al'ummai ne ko mutumin Yahuda, mai kaciya ne ko marar kaciya, baƙo, baƙauye, bawa ne ko 'yantacce, gama Kiristi shi ne kome, kuma yana cikin kome.

12 Da yake Allah ya mai da ku zaɓaɓɓu, tsarkaka, ƙaunatattu, sai ku dinga jin tausayin juna, kuna yin alheri, kuna nuna tawali'u da sauƙinkai da jimrewa. 13 Ku riƙa yin haƙuri da juna kuna kuma gafarta wa juna duk wani laifin da wani ya yi muku. Ku gafarta kamar yadda Ubangiji ya gafarce ku. 14 Fiye da waɗannan duka, ku yi ƙaunar juna, gama ƙauna ce take haɗa kome gaba ɗaya.

15 Ku bar salamar Kiristi tă yi mulki a zukatanku, da yake a matsayin gaɓoɓin jiki ɗaya an kira ku ga salama. Ku zama masu godiya. 16 Ku bar maganar Kiristi ta zauna a cikinku a yalwace yayinda kuke koya, kuna kuma yi wa juna gargaɗi da dukan hikima, da kuma yayinda kuke waƙoƙin zabura, waƙoƙi da waƙoƙin ruhaniya tare da godiya a zukatanku ga Allah. 17 Kuma ko mene ne kuke yi, ko cikin magana ko cikin ayyuka, ku yi shi duka a cikin sunan Ubangiji Yesu, kuna yin godiya ga Allah Uba ta wurinsa.

*Umarnai don iyalan masu bi*

18 Mata, ku yi biyayya ga mazanku, yadda ya dace cikin Ubangiji.

19 Maza, ku ƙaunaci matanku kada ku nuna musu hali marar tausayi.

20 'Ya'ya, ku yi biyayya ga iyayenku cikin kome, gama wannan yakan gamshi Ubangiji.

---

* **3:4** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da ranmu † **3:6** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na farko-farko suna da zuwa a kan waɗanda suke rashin biyayya

21 Ubanni, kada ku matsa wa yaranku lamba, don kada su fid da zuciya.
22 Bayi, ku yi biyayya ga iyayengijinku na duniya cikin kome; kada ku yi aikin
ganin ido kamar masu neman yabon mutane, sai dai ku yi aiki tsakaninku da Allah,
kamar masu tsoron Ubangiji. 23 Kome kuke yi, ku yi shi da dukan zuciyarku, sai ka
ce ga Ubangiji kuke yi, ba ga mutum ba. 24 Kun san cewa zai ba ku gādo a matsayin
ladanku. Ubangiji Kiristi ne fa kuke bauta wa. 25 Duk wanda ya yi laifi, za a sāka
masa don laifinsa, babu sonkai.

# 4

1 Masu bayi, ku riƙe bayinku da kyau da kuma daidai, domin kun san cewa ku ma
kuna da Ubangiji a sama.

*Karin umarnai*

2 Ku nace da yin addu'a, kuna zaman tsaro da kuma godiya. 3 Ku kuma yi mana
addu'a, mu ma, don Allah yă buɗe ƙofa saboda saƙonmu, don mu iya yin shelar asirin
Kiristi, wanda saboda shi nake cikin sarƙoƙi. 4 Ku yi addu'a yadda zan yi shelarsa,
yadda ya kamata. 5 Ku zama masu hikima a yadda kuke ma'amala da waɗanda suke
ba masu bi ba; ku kuma yi amfani da kowane zarafi. 6 Bari maganarku kullum ta
zama da ladabi da kuma daɗin ji, domin ku san amsar da ta dace ku ba wa kowa.

*Gaisuwa ta ƙarshe*

7 Tikikus shi ne ƙaunataccen ɗan'uwan nan, wanda ya yi aiki da aminci a hidimar
Ubangiji tare da mu, zai kuwa faɗa muku dukan labari game da ni. 8 Ina aikansa
shi a gare ku musamman domin ku san yadda muke, yă kuma ƙarfafa muku zuciya.
9 Yana zuwa tare da Onesimus, ƙaunatacce da kuma amintaccen mai bin nan, wanda
yake ɗaya daga cikinku. Za su gaya muku dukan abin da yake faruwa a nan.

10 Aristarkus yana a kurkuku tare da ni. Yana gaishe ku, haka ma Markus, wanda
kakansa ɗaya ne da Barnabas. (Shi ne na riga na yi magana a kansa, na ce muku in
ya zo, ku karɓe shi hannu biyu-biyu.)
11 Yesu, wannan da muke kira Yustus, shi ma yana gaisuwa. Waɗannan ne kaɗai
Yahudawa masu bi a cikin abokan aikina saboda mulkin Allah. Sun kuma zama da
taimako a gare ni.
12 Efafaras naku, mai hidimar Kiristi Yesu, yana gaisuwa. Kullum yana addu'a
dominku sosai, don ku san cikakken abin da Allah yake so ku yi don kuma ku yi
shi cikakke. 13 Na tabbatar muku, cewa yana aiki ƙwarai dominku da kuma domin
waɗanda suke a Lawodiseya da Hiyerafolis.
14 Luka ƙaunataccen likitan nan, da kuma Demas suna gaishe ku.
15 Ku miƙa gaisuwata ga 'yan'uwan da suke a Lawodiseya, musamman ga Nimfa
da kuma ikkilisiyar da take taru a gidanta.

16 Bayan an karanta muku wannan wasiƙa, ku tabbata an karanta ta kuma a
ikkilisiyar Lawodiseyawa; ku ma ku karanta wasiƙar da ta zo daga Lawodiseya.

17 Ku faɗa wa Arkiffus yă tabbata ya ƙarasa aikin da ya karɓa cikin Ubangiji.

18 Ni Bulus ne nake rubuta muku wannan gaisuwa da hannuna. Ku tuna da
sarƙoƙina. Alherin Allah yă kasance tare da ku.

# 1 Tessalonikawa

1 Bulus, Sila[*] da Timoti,

Zuwa ga ikkilisiyar Tessalonikawa ta Allah Uba da Ubangiji Yesu Kiristi.

Alheri da salama su kasance tare da ku.[†]

### *Godiya saboda bangaskiyar Tessalonikawa*

2 Kullum muna gode wa Allah dominku duka, muna ambatonku cikin addu'o'inmu.
3 Muna tunawa da aikinku ba fasawa a gaban Allah da Ubanmu ta wurin bangaskiya,
da famar da kuke yi domin ƙauna, da kuma begenku marar gushewa ga Ubangijinmu
Yesu Kiristi.
4 Gama mun sani, 'yan'uwa, ƙaunatattu na Allah, cewa ya zaɓe ku, 5 domin
bishararmu ba tă zo gare ku da kalmomi kawai ba, amma da iko, da Ruhu Mai
Tsarki, da kuma cikakken tabbaci. Kun san irin rayuwar da muka yi a cikinku don
amfaninku. 6 Har kuka zama masu koyi da mu da kuma Ubangiji; duk da tsananin
wahala, kuka karɓi saƙon nan da farin ciki wanda Ruhu Mai Tsarki ya bayar. 7 Ta
haka kuwa kuka zama gurbi ga dukan masu bi a Makidoniya da Akayya. 8 Saƙon
Ubangiji ya fito daga gare ku ne ba a Makidoniya da Akayya kaɗai ba bangaskiyarku
ga Allah ta zama sananne ko'ina. Saboda haka ba ma bukata mu faɗa wani abu a
kai, 9 gama su kansu su suke ba da labari irin karɓar da kuka yi mana. Suna faɗin
yadda kuka juyo ga Allah daga gumaka don ku bauta wa Allah rayayye da kuma na
gaskiya, 10 ku kuma jira dawowar Ɗansa daga sama, wanda ya tasa daga matattu,
Yesu, wanda ya cece mu daga fushi mai zuwa.

## 2

### *Aikin Bulus a Tessalonika*

1 Kun sani, 'yan'uwa, cewa ziyararmu a gare ku ba tă zama a banza ba. 2 Mun
riga mun sha wahala, aka kuma zage mu a Filibbi, kamar yadda kuka sani, amma
da taimakon Allahnmu muka yi ƙarfin hali muka sanar muku bishararsa duk da
matsananciyar gāba. 3 Gama roƙon da muke yi bai fito daga kuskure ko munafunci
ba, ba kuwa ƙoƙari muke yi mu yaudare ku ba. 4 A maimako haka, muna magana
ne kamar mutanen da Allah ya amince yă danƙa musu amanar wannan bishara. Ba
ma ƙoƙari mu gamshi mutane sai dai Allah, mai auna zukatanmu. 5 Kun san ba ma
taɓa yin daɗin baki ko mu yi ƙoƙarin kasance da halin kwaɗayin da muke ɓoyewa,
Allah shi ne shaidarmu. 6 Ba ma neman yabo daga wurin mutane, ko a gare ku, ko
ga waɗansu.
A matsayinmu na manzannin Kiristi da mun so, da mun nawaita muku, 7 amma
muka kasance masu sauƙinkai a cikinku, kamar yadda mahaifiya take lura da
ƙananan 'ya'yanta. 8 Muka ƙaunace ku ƙwarai har muka ji daɗin bayyana muku,
ba bisharar Allah kaɗai ba amma har rayukanmu ma, domin kun zama ƙaunatattu
a gare mu. 9 Ba shakka kuna iya tunawa, 'yan'uwa, famarmu da kuma wahalarmu;
mun yi aiki dare da rana don kada mu zama nauyi wa wani yayinda muke muku
wa'azin bisharar Allah.

---

[*] **1:1** Da Girik Silbanus, wani suna na Sila [†] **1:1** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da ku daga Allah Ubanmu da Ubangiji Yesu Kiristi

10 Ku shaidu ne, haka ma Allah, na yadda muka yi zaman tsarki, adalci da kuma
marar aibi a cikinku, ku da kuka ba da gaskiya. 11 Gama kun san cewa mun bi
da kowannenku yadda mahaifi yakan yi da 'ya'yansa, 12 muna ƙarfafa ku, muna
ta'azantar da ku, muna kuma gargaɗe ku ku yi rayuwar da za tă cancanci Allah,
wanda ya kira ku zuwa mulkinsa da kuma ɗaukakarsa.

13 Muna kuma gode wa Allah ba fasawa domin, sa'ad da kuka karɓi maganar
Allah, wadda kuka ji daga gare mu, kun karɓe ta ba kamar maganar mutane ba,
sai dai kamar yadda take, maganar Allah wadda take aiki a cikinku ku da kuka ba da
gaskiya. 14 Gama ku, 'yan'uwa, kun zama masu koyi da ikkilisiyoyin Allah a Yahudiya
waɗanda suke cikin Kiristi Yesu. Kun sha wahala a hannun mutanen ƙasarku kamar
yadda ikkilisiyoyin nan ma suka sha a hannun Yahudawa, 15 waɗanda suka kashe
Ubangiji Yesu da annabawa suka kuma kore mu. Ba sa yin aikin da Allah yake
so, masu gāba ne kuwa da dukan mutane 16 suna ƙoƙarin hana mu yin magana ga
Al'ummai don kada su sami ceto. Ta haka kullum suke ƙara tara tsibin zunubansu.
Fushin Allah ya aukar musu a ƙarshe.

### *Marmarin Bulus na ganin Tessalonikawa*

17 Amma, 'yan'uwa, sa'ad da aka raba mu da ku na ɗan lokaci (a jiki, ba a tunani
ba), daga cikin marmarinmu mai tsanani mun yi duk abin da muke iya yi mu gan ku.
18 Gama mun so mu zo wurinku, tabbatacce ni, Bulus, na yi ƙoƙari sau da sau, amma
Shaiɗan ya hana mu. 19 Gama mene ne begenmu, farin cikinmu, ko kuma rawanin
da zai zama mana abin ɗaukaka a gaban Ubangijinmu Yesu sa'ad da ya dawo? Ba
ku ba ne? 20 Tabbatacce, ku ne ɗaukakarmu da kuma farin cikinmu.

## 3

1 Saboda haka da muka kāsa daurewa, sai muka ga ya fi kyau a bar mu a Atens mu
kaɗai. 2 Muka aiki Timoti, wanda yake ɗan'uwanmu da kuma abokin aikin Allah a
cikin yaɗa bisharar Kiristi, don yă gina ku yă kuma ƙarfafa ku cikin bangaskiyarku,
3 don kada kowa yă raunana ta wurin waɗannan gwaje-gwajen. Kun sani sarai cewa
an ƙaddara mu don waɗannan. 4 Gaskiyar ita ce, sa'ad da muke tare da ku, mun
sha gaya muku cewa za a tsananta mana. Haka kuwa ya faru, kamar dai yadda kuka
sani. 5 Saboda wannan, sa'ad da ban iya jimrewa ba, sai na aika domin in sami
labarin bangaskiyarku, da fata kada yă zama mai jarraban nan ya riga ya jarrabce
ku, ƙoƙarinmu kuma yă zama banza.

### *Rahoton mai ƙarfafawa na Timoti*

6 Amma ga shi yanzu Timoti ya dawo mana daga wurinku ya kuma kawo labari mai
daɗi game da bangaskiyarku da kuma ƙaunarku. Ya faɗa mana yadda kullum kuke
da tunani mai kyau a kanmu, yadda kuke marmari ku gan mu, kamar dai yadda mu
ma muke marmari mu gan ku. 7 Saboda haka 'yan'uwa, cikin dukan damuwarmu
da tsananinmu an ƙarfafa mu game da ku saboda bangaskiyarku. 8 Gama yanzu
tabbatacce muna da rai, da yake kuna nan tsaye daram a cikin Ubangiji. 9 Wace irin
godiya ce za mu yi wa Allah saboda ku a kan dukan farin cikin da muke da shi a
gaban Allahnmu ta dalilinku? 10 Dare da rana muna addu'a da himma domin mu
sāke ganinku, mu kuma ba ku abin da kuka rasa a bangaskiyarku.

11 Yanzu bari Allahnmu da Ubanmu kansa da kuma Ubangijinmu Yesu yă shirya
mana hanya mu zo wurinku. 12 Ubangiji yă sa ƙaunarku ta ƙaru ta kuma yalwata ga
juna da kuma ga kowa, kamar yadda tamu take muku. 13 Bari yă ƙarfafa zukatanku
har ku zama marasa aibi da kuma tsarkaka a gaban Allahnmu da Ubanmu sa'ad da
Ubangijimmu Yesu ya dawo tare da dukan tsarkakansa.

# 4

*Rayuwa don a gamshi Allah*
1 A ƙarshe, ʼyanʼuwa, mun umarce ku yadda za ku yi rayuwa domin ku gamshi
Allah, kamar yadda kuke yi. Yanzu muna roƙonku muna kuma gargaɗe ku a cikin
Ubangiji Yesu ku yi haka sau da sau. 2 Gama kun san umarnan da muka ba ku ta
wurin ikon Ubangiji Yesu.
3 Nufin Allah ne a tsarkake ku, cewa ku guje wa fasikanci; 4 don kowannenku yǎ
koya yadda zai ƙame kansa a hanyar da take mai tsarki, mai mutunci kuma, 5 ba
cikin muguwar shaʼawa kamar ta marasa bangaskiya, waɗanda ba su san Allah ba;
6 cikin wannan alʼamari kuwa kada wani yǎ yi wa ɗanʼuwansa laifi ko yǎ cuce shi.
Ubangiji zai hukunta mutane saboda dukan irin waɗannan zunubai, kamar yadda
muka riga muka gaya muku, muka kuma yi muku gargaɗi. 7 Gama Allah bai kira mu
ga zaman marasa tsarki ba, sai dai ga zaman tsarki. 8 Saboda haka, duk wanda ya
ƙi wannan umarni ba mutum ne ya ƙi ba sai ko Allah, wanda ya ba ku Ruhunsa Mai
Tsarki.
9 Yanzu kuwa game da ƙaunar ʼyanʼuwa, ba ma bukata mu rubuta muku, gama ku
kanku Allah ya riga ya koya muku ku ƙaunaci juna. 10 Gaskiyar kuwa ita ce, kuna
ƙaunar dukan ʼyanʼuwa koʼina a Makidoniya. Duk da haka muna ƙara gargaɗe ku,
ʼyanʼuwa, ku yi haka sau da sau. 11 Ku mai da wannan burinku na yi natsattsiyar
rayuwa, kuna mai da hankali ga shaʼanin da yake gabanku, kuna kuma yin aiki da
hannuwanku, kamar dai yadda muka gaya muku, 12 don rayuwanku ta kullum ta
zama da mutunci ga waɗanda suke na waje don kuma kada ku dogara a kan kowa.

*Zuwan Ubangiji*
13 ʼYanʼuwa, ba ma so ku kasance cikin jahilci game da waɗanda suka yi barci, ko
kuwa ku yi baƙin ciki kamar sauran mutanen da ba su da bege. 14 Mun gaskata cewa
Yesu ya mutu ya tashi kuma daga matattu, ta haka muka gaskata cewa Allah zai kawo
waɗanda suka yi barci a cikinsa tare da Yesu. 15 Bisa ga maganar Ubangiji kansa,
muna gaya muku cewa mu da muke raye har yanzu, waɗanda aka bari har dawowar
Ubangiji, tabbatacce ba za mu riga waɗanda suka yi barci tashi ba. 16 Gama Ubangiji
kansa zai sauko daga sama, da umarni mai ƙarfi, da muryar babban malaʼika da
kuma busar ƙahon Allah, waɗanda suka mutu kuwa cikin Kiristi za su tashi da farko.
17 Bayan haka, mu da muke da rai da aka bari, za a ɗauke mu tare da su a cikin
gizagizai don mu sadu da Ubangiji a sararin sama. Ta haka za mu kasance tare da
Ubangiji har abada. 18 Saboda haka ku ƙarfafa juna da waɗannan kalmomi.

# 5

1 To, ʼyanʼuwa, game da lokuta da ranaku, ba ma bukata mu rubuta muku, 2 gama
kun sani sarai cewa ranar Ubangiji za tǎ zo kamar ɓarawo da dare. 3 Yayinda mutane
suke cewa, “Akwai salama da zaman lafiya,” hallaka za tǎ auko musu farat ɗaya,
kamar yadda naƙuda take kama mace mai ciki, ba za su kuwa tsira ba.
4 Amma ku, ʼyanʼuwa, ba kwa cikin duhu da wannan rana za tǎ zo muku ba zato
kamar ɓarawo. 5 Dukanku ʼyaʼyan haske ne da kuma ʼyaʼyan rana. Mu ba mutanen
dare ko na duhu ba ne. 6 Saboda haka fa, kada mu zama kamar saura, waɗanda
suke barci, sai dai mu zama masu tsaro da masu kamunkai. 7 Gama masu barci, da
dad dare suke barci, masu sha su bugu kuwa, da dad dare suke buguwa. 8 Amma da
yake mu na rana ne, bari mu zama masu kamunkai, sanye da bangaskiya da ƙauna
kamar sulke, begen cetonmu kuma kamar hular kwano. 9 Gama Allah bai naɗa mu
don mu sha fushi ba, sai dai mu sami ceto ta wurin Ubangijinmu Yesu Kiristi. 10 Ya
mutu saboda mu domin, ko muna a faɗake ko muna barci, mu kasance tare da shi.
11 Saboda haka ku ƙarfafa juna ku kuma gina juna, kamar dai yadda kuke yi.

*Umarnai na ƙarshe*
12 To, muna roƙonku, ʼyanʼuwa, ku girmama waɗanda suke aiki sosai a cikinku,
waɗanda suke bisanku cikin Ubangiji da kuma waɗanda suke yin muku gargaɗi.
13 Ku riƙe su da mutunci sosai cikin ƙauna saboda aikinsu. Ku yi zaman lafiya da
juna. 14 Muna kuma gargaɗe ku, ʼyanʼuwa, ku gargaɗe waɗanda suke zaman banza,
ku ƙarfafa masu raunanar zuciya, ku taimaki marasa ƙarfi, ku yi haƙuri da kowa.
15 Ku tabbata cewa kada kowa yǎ rama mugunta da mugunta, sai dai kullum ku yi
ƙoƙarin yin wa juna alheri da kuma dukan mutane.
16 Ku riƙa farin ciki kullum; 17 ku ci gaba da yin adduʼa; 18 ku yi godiya cikin kowane
hali, gama wannan shi ne nufin Allah dominku cikin Kiristi Yesu.
19 Kada ku danne aikin Ruhu. 20 Kada ku rena annabci, 21 amma ku gwada kome,
ku riƙe abin da yake mai kyau, 22 ku ƙi kowace mugunta.
23 Bari Allah da kansa, Allah na salama, yǎ tsarkake ku sarai. Bari dukan ruhunku,
ranku, da kuma jikinku su zama marar aibi a dawowar Ubangijinmu Yesu Kiristi.
24 Wannan wanda ya kira ku mai aminci ne zai kuwa aikata.

25 ʼYanʼuwa, ku yi mana adduʼa.

26 Ku gaggai da dukan ʼyanʼuwa da sumba mai tsarki.

27 Na gama ku da Ubangiji ku sa a karanta wannan wasiƙa ga dukan ʼyanʼuwa.

28 Alherin Ubangijinmu Yesu Kiristi yǎ kasance tare da ku.

# 2 Tessalonikawa

1 Bulus, da Sila, da Timoti,

Zuwa ga ikkilisiya ta Tessalonikawa ta Allah Ubanmu da Ubangiji Yesu Kiristi.

2 Alheri da salama daga Allah Uba da kuma Ubangiji Yesu Kiristi, su kasance tare da ku.

### *Godiya da addu'a*

3 Dole kullum mu gode wa Allah saboda ku, 'yan'uwa, haka kuwa ya dace, domin
bangaskiyarku tana girma gaba-gaba, ƙaunar da kowannenku yake yi wa juna kuwa
tana ƙaruwa. 4 Saboda haka, a cikin ikkilisiyoyin Allah muna taƙama game da
daurewarku da kuma bangaskiyarku cikin dukan tsanani da gwaje-gwajen da kuke
sha.
5 Dukan wannan yana tabbatar cewa hukuncin Allah daidai ne, saboda haka kuma
za a lissafta ku a kan kun cancanci mulkin Allah, wanda dominsa ne kuke shan
wahala. 6 Allah mai adalci ne, Zai sāka wa masu ba ku wahala da wahala 7 yǎ kuma
sauƙaƙa muku ku da kuke wahala, har ma da mu. Wannan zai faru sa'ad da aka
bayyana Ubangiji Yesu daga sama cikin wuta mai ci tare da mala'ikunsa masu iko.
8 Zai hukunta waɗanda ba su san Allah ba da kuma waɗanda ba su yi biyayya da
bisharar Ubangijinmu Yesu ba. 9 Za a hukunta su da madawwamiyar hallaka a kuma
kau da su daga gaban Ubangiji da kuma daga ɗaukakar ikonsa 10 a ranar da zai dawo
don a ɗaukaka shi a cikin mutanensa masu tsarki, yǎ kuma zama abin banmamaki
ga dukan waɗanda suka gaskata. Wannan ya haɗa har da ku, domin kun gaskata
shaidar da muka yi muku.
11 Sane da wannan, kullum muna addu'a saboda ku, don Allahnmu yǎ sa ku
cancanci kiransa, ta wurin ikonsa kuma yǎ cika kowace manufarku mai kyau da
kuma kowane aikin da bangaskiyarku ta iza. 12 Muna wannan addu'a don sunan
Ubangijinmu Yesu yǎ sami ɗaukaka a cikinku, ku kuma a cikinsa, bisa ga alherin
Allahnmu da na Ubangiji Yesu Kiristi.*

## 2

### *Mutumin tawayen nan*

1 Game da dawowar Ubangijinmu Yesu Kiristi da game da tattara mu gare shi,
muna roƙonku, 'yan'uwa, 2 kada ku yi saurin jijjiguwa ko kuwa hankalinku yǎ tashi
ta wurin wani annabci, rahoto ko wasiƙar da an ce daga wurinmu ne, cewa ranar
Ubangiji ta riga ta zo. 3 Kada ku bar wani yǎ ruɗe ku ko ta yaya, gama wannan
rana ba za tǎ zo ba sai an yi tawayen nan an kuma bayyana mutumin tawayen nan,
mutumin da aka ƙaddara ga hallaka. 4 Zai yi gāba yǎ kuma ɗaukaka kansa a bisa
kome da ya shafe sunan Allah, ko kuma ake yi wa sujada, domin yǎ kafa kansa a
haikalin Allah, yana shelar kansa a kan shi Allah ne.
5 Ba ku tuna ba cewa sa'ad da nake tare da ku nakan gaya muku waɗannan
abubuwa? 6 Yanzu kuwa kun san abin da yake hana shi, wannan yana faruwa ne
don a bayyana shi a daidai lokaci. 7 Gama ikon asirin tawaye ya riga ya fara aiki; sai
dai wannan da yake hana shi zai ci gaba da yin haka sai an kau da shi. 8 Sa'an nan za
a bayyana mai tawayen, Ubangiji Yesu kuwa zai hamɓare shi da numfashin bakinsa

* **1:12** Ko kuwa Allah da Ubangiji, Yesu Kiristi

yă kuma hallaka shi da darajar dawowarsa. 9 Zuwan mai tawayen nan zai zama ta
wurin aikin Shaiɗan da aka bayyana cikin kowane irin ayyukan banmamaki, alamu
da abubuwan banmamaki na ƙarya, 10 da kuma cikin kowace irin muguntar da take
ruɗin waɗanda suke hallaka. Sun hallaka ne domin sun ƙi su ƙaunaci gaskiya don
su sami ceto. 11 Saboda haka Allah zai aiko musu da babban ruɗu don su gaskata
ƙarya 12 don kuma a hukunta dukan waɗanda ba su gaskata gaskiyar ba sai dai suke
jin daɗin mugunta.

### *A tsaya daram*

13 Amma dole kullum mu gode wa Allah dominku, 'yan'uwa waɗanda Ubangiji
ya ƙaunace, domin daga farko Allah ya zaɓe ku don a cece ku ta wurin aikin
tsarkakewar Ruhu da kuma ta wurin gaskatawa da gaskiya. 14 Ya kira ku ga wannan
ta wurin bishararmu, don ku sami rabo a cikin ɗaukakar Ubangijinmu Yesu Kiristi.
15 Saboda haka fa, 'yan'uwa, sai ku tsaya daram ku riƙe koyarwar da muka miƙa
muku, ko ta wurin maganar baki ko kuma ta wurin wasiƙa.
16 Ubangijinmu Yesu Kiristi kansa da kuma Allah Ubanmu, wanda ya ƙaunace mu
kuma ta wurin alherinsa yă ba mu madawwamiyar ƙarfafawa da kyakkyawar bege,
17 yă ƙarfafa zukatanku yă kuma gina ku cikin kowane aikin nagari da kuma magana.

## 3

### *Roƙo don addu'a*

1 A ƙarshe, 'yan'uwa, ku yi mana addu'a domin saƙon Ubangiji yă yi saurin bazuwa
a kuma girmama shi, kamar yadda yake a wurinku. 2 Ku kuma yi addu'a yadda
za a cece mu daga mugayen mutane masu mugunta, gama ba kowa ba ne yake da
bangaskiya. 3 Ubangiji mai aminci ne, zai ƙarfafa ku, yă kuma tsare ku daga mugun
nan. 4 Muna da tabbaci cikin Ubangiji cewa kuna bin umarnai da muka yi muku,
za ku kuma ci gaba da yin abubuwan da muka umarta. 5 Bari Ubangiji yă bi da
zukatanku ga ƙaunan nan ta Allah da kuma jimirin nan na Kiristi.

### *Gargaɗi game da zaman banza*

6 A cikin sunan Ubangiji Yesu Kiristi, muna muku umarni, 'yan'uwa, da ku kiyaye
kanku daga kowane ɗan'uwa mai zaman banza da ba ya rayuwa bisa ga koyarwar*
da kuka karɓa daga wurinmu. 7 Gama ku kanku kun san yadda ya kamata ku bi
gurbinmu. Ba mu yi zaman banza sa'ad da muke tare da ku ba, 8 ba mu kuwa ci
abincin kowa ba tare da ba mu biya ba. A maimakon haka, mun yi aiki dare da
rana, muna fama muna wahala kuma don kada mu nawaita wa waninku. 9 Mun yi
wannan, ba don ba mu da 'yancin karɓar irin taimakon nan ba ne, sai dai domin mu
zama gurbin da za ku bi. 10 Ko ma a sa'ad da muke tare da ku, mun ba ku wannan
umarni cewa, "In mutum ya ƙi yin aiki, kada a ba shi abinci."
11 Mun ji cewa waɗansunku suna zaman banza. Ba sa aikin kome; sai shisshigi
kurum. 12 Irin waɗannan mutane muna ba da umarni muna kuma gargaɗe su cikin
Ubangiji Yesu Kiristi su natsu su kuma nemi abincin da suke ci. 13 Game da ku kuma
'yan'uwa, kada ku gaji da yin abin da yake daidai.
14 In wani bai yi biyayya da umarninmu a wannan wasiƙa ba, sai fa ku lura da shi.
Kada ku haɗa kai da shi, don yă ji kunya. 15 Duk da haka kada ku mai da shi abokin
gāba, sai dai ku gargaɗe shi a matsayin ɗan'uwa.

### *Gaisuwa ta musamman*

* **3:6** Ko kuwa al'ada

16 Yanzu, bari Ubangiji mai salama kansa yă ba ku salama a kowane lokaci da kuma a ta kowace hanya. Ubangiji yă kasance tare da ku duka.

17 Ni, Bulus, nake rubuta wannan gaisuwa da hannuna, wannan ce shaida a kowace wasiƙata, haka nake rubutu.

18 Alherin Ubangijinmu Yesu Kiristi yă kasance tare da ku duka.

# 1 Timoti

1 Bulus, manzon Kiristi Yesu ta wurin umarnin Allah Mai Cetonmu da kuma na
Yesu Kiristi begenmu,

2 Zuwa ga Timoti ɗana na gaske cikin bangaskiya.

Alheri, jinƙai da kuma salama daga Allah Uba da Kiristi Yesu Ubangijinmu, su
kasance tare da kai.

### *Gargaɗi game da malaman ƙarya*

3 Kamar yadda na gargaɗe ka sa'ad da zan je Makidoniya, ka zauna can Afisa domin
ka umarci waɗansu mutane kada su koyar da ƙa'idodin ƙarya nan gaba 4 ko su ba
da kansu ga tatsuniyoyi da ƙididdigar asali marar iyaka. Waɗannan suna kawo faɗa
a maimakon aikin Allah wanda yake ta wurin bangaskiya. 5 Maƙasudin wannan
umarnin dai ƙauna ce, wadda take zuwa daga zuciya mai tsabta da lamiri mai kyau
da kuma sahihiyar bangaskiya. 6 Waɗansu sun bauɗe daga waɗannan al'amura,
suka koma ga maganganu marasa ma'ana. 7 So suke su zama malaman doka, ba tare
da fahimtar abin da suke faɗa ba, balle abubuwan da suke ta nacewa a kai.
8 Mun san cewa doka tana da kyau in an yi amfani da ita yadda ya kamata. 9 Mun
kuma san cewa an yi doka ba domin masu adalci ba sai dai masu tawaye, da marasa
biyayya, da marasa bin Allah, da masu zunubi, da marasa tsarkaka, da masu saɓon
Allah, da masu kashe iyaye maza da mata, da masu kisankai, 10 da masu zina da kuma
da maza masu kwana da maza, ko mata masu kwana da mata, da masu cinikin bayi
da masu ƙarya da kuma masu shaidar ƙarya, da kuma duk wani abin da ya saɓa
wa sahihiyar koyarwa, 11 da take bisa ga bishara mai ɗaukaka ta Allah mai albarka,
wadda ya danƙa mini.

### *Alherin Ubangiji ga Bulus*

12 Na gode wa Kiristi Yesu Ubangijinmu, wanda ya ba ni ƙarfi, saboda ya amince da
ni, har ya sa ni aikinsa. 13 Ko da yake a dā ni mai saɓo da mai tsanantawa da kuma
mai rikici ne, aka nuna mini jinƙai saboda na yi haka cikin jahilci ne da kuma rashin
bangaskiya. 14 An zubo mini alherin Ubangijinmu a yalwace, tare da bangaskiya da
ƙaunar da take cikin Kiristi Yesu.
15 Ga wata magana tabbatacciya wadda ta cancanci cikakkiyar karɓa. Kiristi Yesu
ya zo duniya domin ceton masu zunubi, wanda nake mafi muni a cikinsu. 16 Amma
saboda wannan dalilin ne aka nuna mini jinƙai domin ta wurina, mafi zunubi duka,
Kiristi Yesu yǎ iya bayyana matuƙar haƙurinsa a matsayin misali ga waɗanda za
su gaskata shi su kuma sami rai madawwami. 17 Bari girma da ɗaukaka su tabbata
har abada abadin ga Sarki madawwami, wanda ba ya mutuwa, wanda ba a ganinsa,
wanda kuma shi ne kaɗai Allah! Amin.
18 Timoti, ɗana, na ba ka wannan umarni bisa ga annabce-annabcen da aka yi
a dā game da kai, domin ta wurin binsu ka iya yin yaƙi mai kyau, 19 kana riƙe
da bangaskiya da kuma lamiri mai kyau. Gama waɗansu mutane, saboda ƙin
kasa kunne ga lamirinsu, suka lalatar da bangaskiyarsu. 20 Cikinsu kuwa akwai
Himenayus da Alekzanda, waɗanda na miƙa ga Shaiɗan don su horo su bar yin
saɓo.

# 2

*Umarnai a kan sujada*

1 Da farko dai, ina gargaɗe ku cewa a yi roƙe-roƙe, ana addu'o'i, ana yin addu'a
a madadin waɗansu da kuma a yi godiya saboda kowane mutum 2 da sarakuna da
dukan masu mulki, domin mu zauna lafiya, rai kuma kwance, muna bin Allah sosai
a cikin natsuwa. 3 Wannan yana da kyau, yakan kuma gamshi Allah Mai Cetonmu,
4 wanda yake so dukan mutane su sami ceto su kuma zo ga sanin gaskiya. 5 Gama
Allah ɗaya ne, matsakanci kuma ɗaya tsakanin Allah da mutane, shi ne kuwa Kiristi
Yesu, 6 wanda ya ba da kansa fansa domin dukan mutane, shaidar da aka bayar a
daidai lokaci. 7 Don haka ne aka sa ni mai wa'azi, da manzo kuma, gaskiya nake faɗa,
ba ƙarya ba, na kuma zama malami mai koya wa al'ummai al'amarin bangaskiya da
kuma na gaskiya.

8 Ina so maza a ko'ina su ɗaga hannuwansu masu tsarki cikin addu'a, ba tare da
fushi ko faɗa ba. 9 Ina kuma so mata su lura su yi wa kansu adon da ya cancanta,
da rigunan da suka dace, ba da adon kitso ko sa kayan zinariya ko lu'ulu'u ko kuma
tufafi masu tsada ba, 10 sai dai su yi ayyuka masu kyan da suka dace da matan da
suke masu bauta wa Allah.
11 Ya kamata mace ta riƙa koyo cikin natsuwa da cikakkiyar biyayya. 12 Ban ba
mace izini ta koyar ko tă yi mulki a kan namiji ba; sai dai ta zauna shiru. 13 Gama
Adamu ne aka fara halitta, sa'an nan Hawwa'u. 14 Ba kuma Adamu ne aka yaudara
ba; macen ce aka yaudara ta kuma zama mai zunubi. 15 Amma mata* Za tă sami
ceto† za su sami ceto ta wurin haihuwa, in suka ci gaba cikin bangaskiya, ƙauna da
kuma tsarki tare da halin sanin ya kamata.

# 3

*Masu kula da ikkilisiya da masu hidimar ikkilisiya*

1 Ga wata tabbatacciyar magana. In wani ya sa zuciyarsa a kan zama mai kula da
ikkilisiya,* yana marmarin yin aiki mai daraja ne. 2 To, dole mai kula da Ikkilisiya yă
kasance marar abin zargi, mijin mace guda, mai sauƙinkai, mai kamunkai, wanda
ake girmama, mai karɓan baƙi, mai iya koyarwa, 3 ba mai buguwa ba, ba mai rikici
ba sai dai mai hankali, ba mai yawan faɗa ba, ba kuma mai yawan son kuɗi ba.
4 Dole yă iya tafiyar da iyalinsa da kyau, yă kuma tabbata cewa 'ya'yansa suna yin
masa biyayya da ladabin da ya dace. 5 (In mutum bai san yadda zai tafiyar da iyalinsa
ba, yaya zai iya kula da ikkilisiyar Allah?) 6 Kada yă zama sabon tuba, in ba haka zai
zama mai girman kai yă kuma fāɗa cikin irin hukuncin da ya fāɗo wa Iblis. 7 Dole
kuma yă kasance da shaida mai kyau ga waɗanda suke na waje, don kada yă zama
abin kunya yă kuma fāɗa cikin tarkon Iblis.

8 Haka masu hidima a cikin ikkilisiya; su ma, su zama maza da sun cancanci
girmamawa, masu gaskiya, ba masu yawan shan ruwan inabi ba, ba masu kwaɗayin
ƙazamar riba ba. 9 Dole su riƙe asirin bangaskiya su kuma kasance da lamiri mai
tsabta. 10 Dole a fara gwada su tukuna; sa'an nan in ba a sami wani abin zargi game
da su ba, sai su shiga aikin masu hidima.

11 A haka kuma, dole matansu su zama matan da suka cancanci girmamawa, ba
masu gulma ba, sai dai masu sauƙinkai da kuma masu aminci a cikin kome.

12 Dole mai hidimar ikkilisiya yă zama mijin mace guda dole kuma yă iya tafiyar da
'ya'yansa da kuma iyalinsa da kyau. 13 Waɗanda suke hidima da kyau suna samar

* 2:15 Da Girik ita † 2:15 Ko kuwa maido * 3:1 A al'adance bishob; haka ma a aya 2

wa kansu kyakkyawan suna da kuma cikakken tabbatarwa a cikin bangaskiyarsu
cikin Kiristi Yesu.
14 Ko da yake ina sa zuciya zo wurinka nan ba da daɗewa ba, ina rubuta muka
waɗannan umarnai domin, 15 in na yi jinkiri, za ka san yadda ya kamata mutane
su tafiyar da halayensu a cikin jama'ar Allah, wadda take ikkilisiyar Allah rayayye,
ginshiƙi da kuma tushen gaskiya. 16 Ba shakka, asirin addini da girma yake.

Ya† bayyana cikin jiki,
Ruhu ya nuna shi adali ne,
mala'iku suka gan shi,
aka yi wa'azinsa cikin al'ummai,
aka gaskata shi a duniya,
aka ɗauke shi sama cikin ɗaukaka.

# 4

*Umarnai ga Timoti*

1 Ruhu a sarari ya faɗa cewa a kwanakin ƙarshe waɗansu za su watsar da
bangaskiya su bi ruhohi masu ruɗu da kuma abubuwan da aljanu suke koyarwa.
2 Irin koyarwan nan tana zuwa ne daga waɗansu munafukai maƙaryata, waɗanda
aka yi wa lamirinsu kaca-kaca. 3 Suna hana mutane yin aure suna kuma umarce su
kada su ci waɗansu irin abinci, waɗanda Allah ya halitta don waɗanda suka gaskata
suka kuma san gaskiya, su karɓa da godiya. 4 Gama duk abin da Allah ya halitta yana
da kyau, kada kuma a ƙi kome in dai an karɓe shi da godiya, 5 domin an tsarkake shi
ta wurin maganar Allah da kuma addu'a.
6 In ka nuna wa 'yan'uwa waɗannan abubuwa, za ka zama mai hidima mai kyau na
Kiristi Yesu, wanda aka goya cikin gaskiyar bangaskiya da kuma koyarwa mai kyau
wadda ka bi. 7 Ka kiyaye kanka daga tatsuniyoyi na rashin tsoron Allah da labaru
banza na tsofaffin mata; a maimako, ka hori kanka ga zama mai tsoron Allah. 8 Gama
horon jiki yana da amfani, amma tsoron Allah yana da amfani ga kowane abu, yana
da albarka ga rai na yanzu da kuma rai mai zuwa. 9 Wannan magana tabbatacciya
ce wadda ta cancanci cikakkiyar karɓa. 10 Saboda wannan kuwa muke wahala da
kuma fama, domin mun sa begenmu ga Allah mai rai, wanda yake Mai Ceton dukan
mutane, musamman na waɗanda suka ba da gaskiya.
11 Ka umarta ka kuma koyar da waɗannan abubuwa. 12 Kada ka bar wani yă
rena ka domin kai matashi ne, sai dai ka zama gurbi ga masu bi cikin magana, cikin
rayuwa, cikin ƙauna, cikin bangaskiya da kuma cikin zaman tsarki. 13 Kafin in zo,
ka ci gaba da karanta wa mutane Nassi, da yin wa'azi, da kuma koyarwa. 14 Kada ka
yi sakaci da baiwarka, wadda aka ba ka ta wurin saƙon annabci sa'ad da ƙungiyar
dattawa suka ɗibiya hannuwa a kanka.
15 Ka yi ƙwazo cikin waɗannan batuttuwa; ka ba da kanka gaba ɗaya gare su, don
kowa yă ga ci gabanka. 16 Ka kula da rayuwarka da kuma koyarwarka da kyau. Ka
daure a cikinsu, domin in ka yi, za ka ceci kanka da kuma masu sauraronka.

# 5

*Shawara game da gwauraye, dattawa da kuma bayi*

1 Kada ka tsawata wa dattijo, sai dai ka gargaɗe shi a matsayinka. Ka ɗauki samari
a matsayin 'yan'uwanka, 2 tsofaffin mata kuwa sai ka ce uwaye, 'yan mata kuma a
matsayin 'yan'uwa da matuƙar tsarki.

† **3:16** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā suna da Allah

3 Ka girmama gwauraye waɗanda suke cikin bukata ta ainihi. 4 Amma in gwauruwa
tana da ʼyaʼya ko jikoki, to, sai su fara koyon yin ayyukan addininsu ga danginsu, ta
haka za su sāka wa iyayensu da kakanninsu, gama wannan yakan gamshi Allah.
5 Gwauruwa wadda ba ta da kowa da zai taimake ta, za tă sa zuciyarta ga Allah, tana
roƙo da adduʼoʼi dare da rana gare shi don taimako. 6 Amma gwauruwar da take
zaman jin daɗi, matacciya ce tun tana da rai. 7 Ka umarce su game da waɗannan
abubuwa, don su kasance marasa abin zargi. 8 In wani bai kula da danginsa ba,
musamman iyalinsa na kurkusa, ya mūsunta bangaskiya ke nan, ya kuma fi marar
ba da gaskiya muni.

9 Kada a lasafta gwauruwa cikin jerin gwauraye sai ta wuce shekara sittin, ta kuma
yi zaman aminci ga mijinta,* 10 aka kuma santa sosai saboda ayyuka masu kyau,
kamar renon ʼyaʼya, da karɓan baƙi, tana yi wa tsarkaka hidima, tana taimakon
waɗanda suke cikin wahala tana kuma ba da kanta ga yin kowane aikin mai kyau.

11 Game da gwauraye masu ƙuruciya kuwa, kada ka sa su cikin wannan lissafi.
Gama saʼad da shaʼawar jikinsu ta kāsa daurewa game da waʼadin da suka yi da
Kiristi, sai su so yin aure. 12 Ta haka suna jawo wa kansu hukunci, saboda sun karya
alkawarinsu na farko. 13 Ban da haka, sukan koyi zaman banza, suna zirga-zirga
gida-gida. Ba kawai sun zama masu zaman banza ba, har ma sun zama masu gulma
da masu shisshigi, suna faɗin abubuwan da bai kamata su faɗa ba. 14 Saboda haka
ina ba wa gwauraye masu ƙuruciya shawara su yi aure, su sami ʼyaʼya, su lura da
gidajensu kada kuwa su ba abokin gāba zarafin ɓata suna. 15 Waɗansu dai sun riga
sun bauɗe sun bi Shaiɗan.

16 In mace mai bi tana da gwauraye a iyalinta, ya kamata tă taimake su, kada tă bar
wa ikkilisiya wannan nauyi, domin ikkilisiya ta sami zarafin taimakon gwaurayen da
suke da bukata ta ainihi.

17 Dattawan da suka bi da alʼamuran ikkilisiya da kyau sun cancanci girmamawa
ninki biyu, musamman waɗanda aikinsu waʼazi ne da kuma koyarwa. 18 Gama Nassi
ya ce, “Kada ka sa wa bijimi takunkumi yayinda yake sussukar hatsi,”† da kuma,
“Maʼaikaci ya cancanci hakkinsa.”‡ 19 Kada ka saurari ƙara game da dattijo sai da
shaidu biyu ko uku. 20 Amman waɗannan dattawa waɗanda suke yin zunubi kuwa
sai ka kwaɓe su a gaban jamaʼa, don saura su ji tsoro. 21 Na gama ka da Allah, da
Kiristi Yesu, da kuma zaɓaɓɓun malaʼiku, ka kiyaye waɗannan abubuwa ƙwarai da
gaske, kada ka nuna bambanci.

22 Kada ka yi garajen ɗibiya hannuwa, kada kuma ka yi tarayya a cikin zunuban
waɗansu. Ka kiyaye kanka da tsarki.

23 Ka daina shan ruwa kaɗai, yi amfani da ruwan inabi kaɗan saboda cikinka da
kuma yawan rashin lafiyarka.

24 Zunuban waɗansu mutane a fili suke, suna shan gabansu zuwa hukunci;
zunuban waɗansu kuwa sukan bi su a baya. 25 Haka ma ayyuka nagari a fili suke,
ko ba ma a fili suke ba, ba a iya ɓoye su.

# 6

1 Duk waɗanda suke ƙarƙashin bauta, ya kamata su ɗauki iyayengijinsu a kan sun
cancanci girmamawa matuƙa, don kada a ɓata sunan Allah da kuma koyarwarmu.
2 Waɗanda suke da iyayengiji masu bi, to, kada su yi musu reni domin su ʼyanʼuwa ne.
A maimako, sai ma su fi bauta musu, saboda waɗanda suke cin moriyar hidimarsu
masu bi ne, ƙaunatattu ne kuma a gare su.

*Kaunar kuɗi*

* **5:9** Ko kuwa ta auri miji guda kawai † **5:18** M Sh 25.4 ‡ **5:18** Luk 10.7

Waɗannan su ne abubuwan da za ka koya musu ka kuma gargaɗe su. 3 In wani
yana koyarwar ƙarya bai kuma yarda da sahihiyar koyarwar Ubangijinmu Yesu
Kiristi da kuma koyarwa ta tsoron Allah ba, 4 yana cike da girman kai bai kuma
san kome ba. Yana da mugun halin son gardama da muhawwara game da kalmomin
da suke kawo kishi, rikici, maganar ƙeta, da mugayen zace-zace 5 da yawan tankiya
tsakanin mutane masu mugun hali, waɗanda aka raba su da gaskiya, suke kuma
tsammani cewa bin Allah wata hanya ce ta samun kuɗi.
6 Amma bin Allah da gamsuwa riba ce mai yawa. 7 Gama ba mu zo duniya da kome
ba, ba kuwa za mu fita daga cikinta da kome ba. 8 In dai muna da abinci da sutura,
ai, sai mu gamsu da su. 9 Mutanen da suke son yin arziki sukan fāɗi cikin jarraba,
su fāɗa a tarko, suna mugayen sha'awace-sha'awace iri-iri na wauta da cutarwa, irin
waɗanda suke dulmuyar da mutane, su kai ga lalacewa da hallaka. 10 Gama son kuɗi
shi ne tushen kowane irin mugun abu. Waɗansu mutane, don tsananin son kuɗi, sun
bauɗe daga bangaskiya suka kuma jawo wa kansu da baƙin ciki iri-iri.

### *Umarnin Bulus ga Timoti*

11 Amma kai, mutumin Allah, ka guji duk wannan, ka kuma nemi adalci, tsoron
Allah, bangaskiya, ƙauna, jimrewa da kuma hankali. 12 Ka yi fama, kyakkyawar
fama ta bangaskiya. Ka riƙi rai madawwamin nan, wanda aka kira saboda shi, sa'ad
da ka yi kyakkyawar shaida a gaban shaidu masu yawa. 13 Na umarce ka, a gaban
Allah mai ba da rai ga kome, da kuma Kiristi Yesu wanda yayinda yake ba da shaida
a gaban Buntus Bilatus ya yi kyakkyawar shaida, 14 ka kiyaye wannan umarni ba tare
da wani aibi ko abin zargi ba har yă bayyanuwar Ubangijinmu Yesu Kiristi, 15 wanda
Allah zai kawo a daidai lokaci, Allah, mai albarka wanda yake kaɗai Mai Mulki, Sarkin
sarakuna da Ubangijin iyayengiji, 16 wanda shi kaɗai ne marar mutuwa wanda kuma
yake zaune cikin hasken da ba ya kusatuwa, wanda babu wanda ya taɓa gani ko zai
iya gani. A gare shi girma da iko su tabbata har abada. Amin.
17 Ka umarci waɗanda suke da arziki a wannan duniya kada su ɗaga kai ko su sa
begensu a kan dukiyar da ba ta da tabbaci, sai dai su sa begensu ga Allah, wanda yake
ba mu kome a yalwace don jin daɗinmu. 18 Ka umarce su su yi nagarta, su wadatu
cikin ayyuka nagari, su kuma zama masu bayarwa hannu sake da kuma masu niyyar
yin taimako. 19 Ta haka za su ajiye wa kansu dukiya a matsayin tushen mai ƙarfi don
tsara mai zuwa, don su riƙi rai wanda yake na tabbatacce.
20 Timoti, ka lura da abin da aka danƙa maka amana. Ka yi nesa da masu
maganganun rashin tsoron Allah da kuma yawan mūsu da ake ƙarya, ake ce da shi
ilimi, 21 wanda waɗansu suka furta kuma ta yin haka suka bauɗe daga bangaskiya.

Alheri yă kasance tare da ku.

# 2 Timoti

1 Bulus, manzon Kiristi Yesu ta wurin nufin Allah, bisa ga alkawarin rai wanda yake
cikin Kiristi Yesu,

2 Zuwa ga Timoti, ƙaunataccen ɗana.

Alheri, jinƙai da salama daga Allah Uba da kuma Kiristi Yesu Ubangijinmu, su
kasance tare da kai.

*Godiya*

3 Na gode wa Allah wanda nake bauta wa, kamar yadda kakanni-kakannina suka
yi da lamiri mai tsabta, yadda kullum dare da rana ina tuna da ku a cikin addu'o'ina.
4 Sa'ad da na tuna da hawayenka, nakan yi marmarin ganinka, don in cika da farin
ciki. 5 An tunashe ni da sahihiyar bangaskiyarka, wadda a farko ta kasance a cikin
kakarka Loyis da kuma mahaifiyarka Yunis yanzu kuwa na tabbata tana cikinka.

*Karfafawa don zaman aminci*

6 Saboda haka, ina so in faɗakar da kai, ka lura baiwan nan ta Allah, wadda take
tare da kai ta wurin ɗibiya maka hannuwana. 7 Gama Allah bai ba mu ruhun tsoro
ba, sai dai ruhun iko, na ƙauna da kuma na kamunkai. 8 Saboda haka kada ka ji
kunyar ba da shaida game da Ubangijinmu, ko kuwa ka ji kunyata, ni da nake ɗan
sarƙa saboda shi. Sai dai ka haɗa kai tare da ni cikin shan wahala saboda bishara
ta wurin ikon Allah, 9 wanda ya cece mu ya kuma kira mu ga rayuwar tsarki ba
saboda wani abin da muka yi ba sai dai saboda nufinsa da kuma alherinsa. An ba
mu wannan alheri cikin Kiristi Yesu tun fil azal, 10 amma yanzu an bayyana ta ta
wurin bayyanuwar Mai Cetonmu, Kiristi Yesu, wanda ya hallaka mutuwa ya kuma
kawo rai da rashin mutuwa a sarari ta wurin bishara. 11 A wannan bishara ce, aka
naɗa ni mai shela da manzo da kuma malami. 12 Shi ya sa nake shan wahalar da
nake sha. Duk da haka ba na jin kunya, domin na san wanda na gaskata da shi, na
kuma tabbata cewa yana iya kiyaye abin da na danƙa masa* amana don wancan
rana.
13 Abin da ka ji daga gare ni, ka kiyaye shi kamar tsarin sahihiyar koyarwa, cikin
bangaskiya da ƙauna cikin Kiristi Yesu. 14 Ka kiyaye kyakkyawar ajiyan nan da aka
danƙa maka amana, ka lura da ita da taimakon Ruhu Mai Tsarki wanda yake raye a
cikinmu.
15 Ka san cewa kowa a lardin Asiya ya juya mini baya, har da Figelus da
Hermogenes.
16 Bari Ubangiji yǎ yi wa iyalin Onesiforus jinƙai, domin sau da dama yakan
wartsakar da ni, bai kuma ji kunyar sarƙoƙina ba. 17 A maimakon haka ma, sa'ad da
yake a Roma, ya neme ni ido a rufe sai da ya same ni. 18 Bari Ubangiji yǎ sa yǎ sami
jinƙai daga Ubangiji a wancan ranar! Ka sani sarai yadda ya taimake ni a hanyoyi
dabam-dabam a Afisa.

## 2

1 Kai kuma, ɗana, ka yi ƙarfi cikin alherin da yake cikin Kiristi Yesu. 2 Abubuwan
da ka ji na faɗa a gaban shaidu masu yawa kuwa ka danƙa wa amintattun mutane
waɗanda su ma za su iya koya wa waɗansu. 3 Ka jure wa shan wahala tare da mu
kamar soja mai kyau na Kiristi Yesu. 4 Ba wanda yake aikin soja da zai sa kansa a

* **1:12** Ko kuwa abin da aka danƙa mini

shaʼanin mutumin da ba ya aikin soja, domin yakan so yă gamshi wanda ya ɗauke
shi soja. 5 Haka ma, in wani ya yi gasa a matsayi shi ɗan wasa ne, ba ya sami rawanin
nasara, sai in ya yi gasar bisa ga dokoki. 6 Manomi mai aiki sosai ya kamata yă zama
na fari wajen samun rabon amfanin gona. 7 Ka yi tunani a kan abin da nake faɗi,
gama Ubangiji zai ba ka ganewa cikin dukan wannan.

8 Ka tuna da Yesu Kiristi, wanda aka tā da shi daga matattu, zuriyar Dawuda,
wanda shi ne bisharata, 9 wadda nake shan wahala har ga daurin sarƙa kamar mai
laifi. Amma Maganar Allah ba a daure take ba. 10 Saboda haka nake jure kome
saboda zaɓaɓɓu, domin su ma su sami ceton da yake cikin Kiristi Yesu, tare da
madawwamiyar ɗaukaka.

11 Ga wata magana tabbatacciya,

“In muka mutu tare da shi,
za mu rayu tare da shi;
12 in muka jimre,
za mu yi mulki tare da shi.
In muka yi mūsunsa,
shi ma zai yi mūsunmu;
13 in ba mu da aminci,
shi dai mai aminci ne,
domin shi ba zai iya mūsun kansa ba.”

### *Maʼaikacin da Allah ya amince*

14 Ka riƙa tuna masu da haka, ka kuma gama su da Allah, kada su yi jayayya a
kan maganganu, don ba ta da wani amfani, sai ɓad da masu ji kawai take yi. 15 Ka yi
iyakacin ƙoƙarinka ka gabatar da kanka a gaban Allah a matsayin wanda aka amince
da shi, maʼaikaci wanda ba shi da dalilin jin kunya wanda kuma yake fassara kalmar
gaskiya daidai. 16 Ka yi nesa da maganganun banza na rashin tsoron Allah, gama
waɗanda suka mai da hankali ga yin waɗannan za su ƙara zama marasa tsoron Allah.
17 Koyarwarsu za tă bazu kamar ruɓaɓɓen gyambo. A cikinsu akwai Himenayus da
Filetus, 18 waɗanda suka bauɗe daga gaskiya. Suna cewa tashin matattu ya riga
ya faru, suna kuma ɓata bangaskiyar waɗansu. 19 Duk da haka, ƙaƙƙarfan tushen
nan na Allah yana nan daram, an hatimce shi da wannan rubutu, “Ubangiji ya san
waɗanda suke nasa,”* da kuma, “Duk wanda ya bayyana yarda ga sunan Ubangiji,
to, dole yă yi nesa da aikata mugunta.”

20 A babban gida akwai kayayyakin da ba na zinariya da na azurfa kaɗai ba, amma
har da na katako da na yumɓu ma; waɗansu domin hidima mai daraja waɗansu
kuwa domin hidima marar daraja. 21 In mutum ya tsabtacce kansa daga na farkon
zai zama kayan aikin hidima mai daraja, mai amfani ga Maigida, kuma shiryayye
domin yin kowane aiki mai kyau.

22 Ka yi nesa da mugayen shaʼawace-shaʼawace na ƙuruciya, ka kuma bi adalci,
bangaskiya, ƙauna da kuma salama, tare da waɗanda suke kira ga Ubangiji daga
zuciya mai tsabta. 23 Kada wani abu yă haɗa ka da gardandamin banza da wofi,
domin ka san yadda suke jawo faɗa. 24 Bai kamata bawan Ubangiji yă zama mai
neman faɗa ba; a maimako, dole yă nuna alheri ga kowa, mai iya koyarwa, mai
haƙuri kuma. 25 Waɗanda suke gāba da shi kuwa dole yă yi musu gargaɗi cikin
hankali, da fata Allah zai sa su tuba su kai ga sanin gaskiya, 26 su kuma dawo cikin
hankulansu su kuɓuta daga tarkon Iblis, wanda ya sa suka zama kamammu don su
aikata nufinsa.

* **2:19** Kid 16.5 (dubi Seftuwajin)

# 3

*Rashin sanin Allah a kwanakin ƙarshe*
1 Amma fa ka san wannan, za a yi lokutan shan wahala a kwanakin ƙarshe.
2 Mutane za su zama masu son kansu, masu son kuɗi, masu taƙama, masu girman kai,
masu zage-zage, marasa biyayya ga iyayensu, marasa godiya, marasa tsarki, 3 marasa
ƙauna, marasa gafartawa, masu ɓata sunayen waɗansu, marasa kamunkai, masu
ƙeta, marasa ƙaunar nagarta, 4 masu cin amana, marasa hankali, waɗanda sun cika
da ɗaga kai, masu son jin daɗi a maimakon ƙaunar Allah 5 suna riƙe da siffofin ibada,
amma suna mūsun ikonta. Kada wani abu yă haɗa ka da su.
6 Irin su ne suke saɗaɗawa su shiga gidaje suna rinjayar mata marasa ƙarfin hali,
waɗanda zunubai suka sha kansu, mugayen sha'awace-sha'awace kuma sun ɗauke
hankulansu, 7 kullum suna koyo amma ba sa taɓa iya yarda da gaskiya. 8 Kamar
dai yadda Yannes da Yamberes* suka tayar wa Musa, haka waɗannan mutane ma
suke tayar wa gaskiya, mutane masu ɓataccen hankali, waɗanda, in ana zancen
bangaskiya ne, to, fa ba sa ciki. 9 Sai dai ba za su yi nisa ba, don rashin hankalinsu
zai bayyana ga kowa, kamar na mutanen nan biyu.

*Umarnin Bulus ga Timoti*
10 Kai kam, ka san kome game da koyarwata, da halina, da niyyata, bangaskiya,
haƙuri, ƙauna, jimiri, 11 tsanani, shan wahala, irin abubuwan da suka faru da ni
a Antiyok, Ikoniyum da kuma Listira, tsananin da na jure. Duk da haka Ubangiji
ya cece ni daga dukansu. 12 Labudda, duk masu niyyar zaman tsarkaka, suna na
Kiristi Yesu, za su sha tsanani. 13 Mugayen mutane da masu ruɗi kuwa, ƙara muni
za su riƙa yi, suna yaudara, ana kuma yaudararsu. 14 Amma kai kam, ka ci gaba da
abin da ka koya ka kuma tabbatar, gama ka san waɗanda ka koye su daga gare su,
15 da kuma yadda tun kana ɗan jinjiri ka san Nassosi masu tsarki, waɗanda suke iya
sa ka zama mai hikima zuwa ceto ta wurin bangaskiya cikin Kiristi Yesu. 16 Dukan
Nassi numfashin Allah ne yana kuma da amfani don koyarwa, tsawatarwa, gyara da
kuma horarwa cikin adalci, 17 domin mutumin Allah yă zama shiryayye sosai saboda
kowane kyakkyawan aiki.

# 4

1 A gaban Allah da kuma Kiristi Yesu, wanda zai yi wa masu rai da matattu shari'a,
saboda kuma bayyanuwarsa da mulkinsa, ina ba ka umarni. 2 Ka yi wa'azin Maganar
Allah, ka zama a shirye a kullum, ko da zarafi, ko babu zarafi, ka yi gyara, ka
kwaɓe, ka kuma ƙarfafa, da matuƙar haƙuri da koyarwa cikin natsuwa. 3 Gama
lokaci yana zuwa da mutane ba za su jure da sahihiyar koyarwa ba. A maimako,
don cimma burinsu, za su taro wa kansu malamai masu yawa, domin su faɗi abin da
kunnuwansu masu ƙaiƙayi suke so su ji. 4 Za su juye kunnuwansu daga gaskiya zuwa
ga jin tatsuniyoyi. 5 Amma kai, ka natsu cikin kowane hali, ka jure shan wahala, ka
yi aikin mai bishara, ka cika dukan ayyukan hidimarka.
6 Gama an riga an tsiyaye ni kamar hadaya ta sha, kuma lokacin tashina ya yi. 7 Na
yi fama mai kyau, na gama tseren, na riƙe bangaskiya. 8 Yanzu kuwa an ajiye mini
rawanin adalci, wanda Ubangiji, Alƙali mai adalci zai ba ni a ranan nan ba kuwa ni
kaɗai ba, amma ga duk waɗanda suka yi marmarin bayyanuwarsa.

*Maganar ƙarshe*

* **3:8** Yannes da Yamberes. Babu waɗannan sunaye a Tsohon Alkawari, amma bisa ga masanan tarihin Yahudawa, mutanen nan su ne bokaye biyun nan na ƙasar Masar da suka yi gāba da Musa lokacin da ya so yă fitar da 'ya'yan Isra'ila daga ƙasar Masar (Dubi Fit 7.11,22; 9.11)

[9] Ka yi iyakacin ƙoƙarinka ka zo wurina da sauri, [10] gama Demas, saboda ƙaunar
wannan duniya, ya yashe ni ya tafi Tessalonika. Kirssens ya tafi Galatiya, Titus kuwa
ya tafi Dalmatiya. [11] Luka ne kaɗai yake tare da ni. Ka nemi Markus ku zo tare, domin
yana da amfani a gare ni cikin hidimata. [12] Na aiki Tikikus zuwa Afisa. [13] Sa'ad da
za ka dawo, ka zo mini da alkyabbar da na bari a wurin Karbus a Toruwas, da kuma
naɗaɗɗun littattafaina, tun ba ma fatun nan masu rubutu ba.
[14] Alekzanda maƙerin ƙarafan nan ya yi mini mugunta ƙwarai. Ubangiji zai sāka
masa saboda abin da ya yi. [15] Kai ma sai ka lura da shi, domin ya yi gāba sosai da
saƙonmu.
[16] A lokacin da na kāre kaina da farko, ba wanda ya goyi bayana, sai ma kowa
ya yashe ni. Ina fata ba za a lasafta wannan laifi a kansu ba. [17] Amma Ubangiji ya
tsaya tare da ni, ya kuma ba ni ƙarfi, don ta wurina a yi cikakkiyar shelar saƙon har
Al'ummai duka su ji. Aka kuma cece ni daga bakin zaki. [18] Ubangiji zai cece ni daga
kowane mugun hari yă kuma kai ni mulkinsa na sama lafiya. A gare shi ɗaukaka ta
tabbata har abada abadin. Amin.

*Gaisuwa ta ƙarshe*

[19] Ka gai da Firiskila da Akwila da iyalin Onesiforus.

[20] Erastus ya dakata a Korint, na kuma bar Turofimus cikin rashin lafiya a Miletus.
[21] Ka yi iyakacin ƙoƙarinka ka iso nan kafin damina.

Yubulus yana gaishe ka, haka ma Fuden, Lainus, Kalaudiya da kuma dukan 'yan'uwa.

[22] Ubangiji yă zama tare da ruhunka. Alheri yă zama tare da ku.

# Titus

1 Bulus, bawan Allah da kuma manzon Yesu Kiristi saboda bangaskiyar zaɓaɓɓu
na Allah da kuma sanin gaskiya wadda take kaiwa ga rayuwa ta tsoron Allah 2 duk
wannan kuwa saboda begen nan ne ga rai madawwami da Allah ya yi alkawari tun
fil azal, shi wanda ƙarya ba ta a gare shi, 3 da lokacin da Allah ya zaɓa ya cika sai
ya bayyana maganarsa a sarari ta wurin wa'azin da aka danƙa mini amana ta wurin
umarnin Allah Mai Cetonmu,

4 Zuwa ga Titus, ɗana na gaske a tarayyarmu cikin bangaskiya.

Alheri da salama daga Allah Uba da kuma Kiristi Yesu Mai Cetonmu, su kasance tare da kai.

### *Aikin Titus a Kirit*

5 Dalilin da ya sa na bar ka a Kirit shi ne don ka daidaita abubuwan da suka rage
da ba a kammala ba, ka kuma naɗa dattawa a kowane gari, yadda na umarce ka.
6 Dole dattijo yă kasance marar aibi, mijin mace guda, mutumin da 'ya'yansa masu
bi ne, waɗanda kuma ba a san su da lalata ko rashin biyayya ba. 7 Da yake an danƙa
wa mai kula da ikkilisiya riƙon amana saboda Allah, dole yă zama marar aibi ba mai
girman kai ba, ba mai saurin fushi ba, ba mai buguwa ba, ba mai rikici ba, ba kuma
mai son ƙazamar riba ba. 8 A maimakon haka dole yă zama mai karɓan baƙi, mai
son abu nagari, mai kamunkai, mai adalci, mai tsarki da kuma natsattse. 9 Dole yă
riƙe tabbataccen saƙon nan kam-kam yadda aka koyar, don yă iya ƙarfafa waɗansu
da sahihiyar koyarwa yă kuma ƙaryata waɗanda suke gāba da shi.

### *Tsawata wa waɗanda suka ƙi yin nagarta*

10 Gama akwai 'yan tawaye da yawa, masu surutun banza da masu ruɗi,
musamman ƙungiyar masu kaciya. 11 Dole a hana su yin magana, domin suna
kawo rushewar iyalai ta wurin koyar da abubuwan da bai kamata su koyar ba
don neman ƙazamar riba. 12 Wani daga cikin annabawansu ma ya ce, "Kiretawa a
kullum maƙaryata ne, mugayen dabbobi, ragwaye haɗamammu." 13 Wannan shaida
gaskiya ce. Saboda haka, sai ka tsawata musu sosai, don su zama sahihai a wajen
bangaskiya, 14 ba za su kuma mai da hankalinsu ga tatsuniyoyin Yahudawa ko ga
umarnan waɗanda suke ƙin gaskiya ba. 15 Ga tsarkaka kuwa, kome mai tsarki ne,
amma ga waɗanda suke marasa tsarki da kuma marasa ba da gaskiya, ba abin da
yake da tsarki. Gaskiya dai, hankulansu da lamirinsu duk marasa tsarki ne. 16 Sun
ɗauka cewa sun san Allah, amma ta wurin ayyukansu suna mūsunsa. Sun zama
abin ƙyama, marasa biyayya, ba su ma isa su yi aiki nagari ba.

## 2

### *Abin da ya kamata a koyarwa wa ƙungiyoyi dabam-dabam*

1 Dole ka koyar da abin da yake bisa sahihiyar koyarwa. 2 Ka koya wa tsofaffin maza
su kasance masu sauƙinkai, waɗanda suka cancanci girmamawa, masu kamunkai,
sahihai wajen bangaskiya, da ƙauna da kuma jimiri.
3 Haka ma, ka koya wa tsofaffin mata su zama masu bangirma cikin rayuwarsu, ba
masu ɓata suna ko masu jarrabar shan giya ba, sai dai su zama masu koyar da abin
da yake nagari. 4 Sa'an nan za su iya su koya wa mata masu ƙuruciya su ƙaunaci

mazansu da ʼyaʼyansu, [5] su kasance da kamunkai da kuma tsarki, masu aiki a gida,
masu kirki da kuma masu biyayya ga mazansu, don kada wani yă rena maganar
Allah.
[6] Haka kuma, ka ƙarfafa samari su zama masu kamunkai. [7] Cikin kowane abu ka
zama musu misali mai kyau ta wurin aikata abin da yake nagari. A cikin koyarwarka
ka nuna mutunci da ƙwazo [8] da kuma sahihanci cikin maganar da ba za a iya kushewa
ba, domin masu gāba da kai su ji kunya, su kuma rasa wani mugun abin da za su
faɗa game da mu.
[9] Ka koya wa bayi su yi wa iyayengijinsu biyayya cikin kowane abu, su yi ƙoƙari
su gamshe su, kada su mayar musu da magana, [10] kada kuma su yi musu sata, sai
dai su nuna za a iya amince da su sosai, don ta kowace hanya su sa koyarwa game
da Allah Mai Cetonmu ta zama abin ɗaukan hankali.
[11] Gama alherin Allah mai kawo ceto ya bayyana ga dukan mutane. [12] Yana koya
mana mu ce, "Aʼa" ga rashin tsoron Allah da kuma shaʼawace-shaʼawacen duniya,
mu kuma yi rayuwa ta kamunkai, ta adalci da kuma ta tsoron Allah a cikin wannan
zamani, [13] yayinda muke sauraron begenmu mai albarka bayyanuwar ɗaukakar
Allahnmu mai girma da kuma Mai Cetonmu, Yesu Kiristi, [14] wanda ya ba da kansa
dominmu don yă fanshe mu daga dukan mugunta yă kuma tsarkake wa kansa
mutanen da suke nasa, waɗanda suke marmarin yin abin da yake nagari.
[15] Waɗannan kam, su ne abubuwan da ya kamata ka koyar, ka ƙarfafa ka kuma
tsawata da dukan iko. Kada ka yarda wani yă rena ka.

# 3

*Yin abin da yake mai kyau*

[1] Ka tuna wa mutane su zama masu biyayya ga masu mulki da kuma hukumomi, su
zama masu biyayya suna kuma a shirye su yi kowane abin da yake mai kyau, [2] kada
su zama masu ɓata sunan kowa, su zama masu salama da kulawa, su kuma zama
masu matuƙar tawaliʼu ga dukan mutane.
[3] A wani lokaci can baya mu ma wawaye ne, marasa biyayya, aka ruɗe mu,
shaʼawace-shaʼawace da kwaɗayi iri-iri suka daure mu, muka yi zaman ƙiyayya da
kishi, aka ƙi mu, mu kuma muka ƙi juna. [4] Amma da alheri da kuma ƙaunar Allah
Mai Cetonmu suka bayyana, [5] sai ya cece mu, ba saboda abubuwan adalcin da muka
aikata ba, sai dai saboda jinƙansa. Ya cece mu ta wurin wankan nan na sāke haihuwa
da kuma sabuntawan nan ta Ruhu Mai Tsarki, [6] wanda ya zubo mana a yalwace ta
wurin Yesu Kiristi Mai Cetonmu, [7] wannan fa domin an kuɓutar da mu ne ta wurin
alherinsa, don mu zama magāda masu begen ga rai madawwami. [8] Wannan magana
tabbatacciya ce, ina kuma so ka nanata waɗannan abubuwa ƙwarai, domin waɗanda
suka dogara ga Allah su himmantu ga aiki mai kyau. Waɗannan abubuwa suna da
kyau sosai suna kuma da amfani ga kowane mutum.
[9] Amma ka guji jayayyar banza da ƙididdigar asali da gardandami da faɗace-faɗace
game da Doka, gama ba su da riba kuma aikin banza ne. [10] Ka gargaɗe mutumin da
yake kawo tsattsaguwa sau ɗaya, ka kuma gargaɗe shi sau na biyu. Bayan haka,
kada wani abu yă haɗa ka da shi. [11] Ka dai san cewa irin mutumin nan ya taurare
kuma mai zunubi ne; ya yanke wa kansa hukunci.

*Maganar ƙarshe*

[12] Da zarar na aika Artemas ko Tikikus zuwa wurinka, sai ka yi iyakacin ƙoƙarinka
ka zo wurina a Nikofolis, domin na yanke shawara in ci damina a can. [13] Ka yi
iyakacin ƙoƙarinka ka taimaki Zenas lauyan nan da Afollos a hanyarsu ka kuma
tabbata ba su rasa kome ba.

14 Dole mutanenmu su koyi ba da kansu ga aikata abin da yake nagari, domin su
iya biyan bukatunsu na yau da kullum kada kuma su yi rayuwar marar amfani.

15 Dukan waɗanda suke tare da ni suna gaishe ka.
Ka gaggai mini da masoyanmu, masu bangaskiya.

Alheri yă kasance tare da ku duka.

# Filemon

1 Bulus, ɗan kurkuku saboda Kiristi Yesu, da kuma Timoti ɗan'uwanmu,

Zuwa ga Filemon ƙaunataccen abokinmu da kuma abokin aikinmu, 2 zuwa kuma
ga Affiya 'yar'uwarmu, zuwa kuma ga Arkiffus abokin famarmu, da zuwa kuma ga
ikkilisiyar da take taruwa a gidanka.

3 Alheri da salama daga Allah Ubanmu da kuma Ubangiji Yesu Kiristi, su kasance
tare da ku.

### *Godiya da addu'a*

4 Kullum nakan gode wa Allahna sa'ad da nake tuna da kai cikin addu'o'ina, 5 domin
ina jin labari bangaskiyarka cikin Ubangiji Yesu da kuma ƙaunarka da kake yi saboda
dukan tsarkaka. 6 Ina addu'a ka zama mai ƙwazo cikin shaida bangaskiyarka, domin
ka sami cikakken fahimta ta kowane abin da yake nagarin da muke da shi cikin
Kiristi. 7 Kaunarka ta sa ni farin ciki ƙwarai ta kuma ƙarfafa ni, domin kai, ɗan'uwa,
ka wartsake zukatan tsarkaka.

### *Roƙon Bulus domin Onisemus*

8 Saboda haka, ko da yake cikin Kiristi ina iya yin ƙarfin hali in umarce ka ka yi
abin da ya kamata, 9 duk da haka ina roƙonka saboda ƙauna, na fi so in roƙe ka,
ni Bulus tsoho, a yanzu kuma ga ni ɗan sarƙa saboda Kiristi Yesu. 10 Ina roƙonka
saboda ɗana Onesimus,* wanda ya zama ɗana yayinda nake cikin sarƙoƙi. 11 Dā
kam, ba shi da amfani a gare ka, amma yanzu ya zama da amfani a gare ka da kuma
gare ni.

12 Ina aike shi yă koma gare ka, shi da yake zuciyata. 13 Na so in riƙe shi a wurina
a madadinka domin yă taimake ni yayinda nake cikin sarƙoƙi saboda bishara. 14 Sai
dai ban so in yi kome ban da yardarka ba, domin kowane alherin da za ka yi, yă fito
daga zuciyarka, ba na tilas ba. 15 Wataƙila abin da ya sa aka raba ka da shi na ɗan
lokaci ƙanƙani shi ne don ka same shi da amfani 16 ba kamar bawa kuma ba, sai dai
fiye da bawa, a matsayin ƙaunataccen ɗan'uwa. Shi ƙaunatacce ne sosai a gare ni
amma a gare ka ya ma fi zama ƙaunatacce, kamar mutum da kuma kamar ɗan'uwa
a cikin Ubangiji.

17 Saboda haka in ka ɗauke ni a kan ni abokin tarayya ne, sai ka marabce shi kamar
yadda za ka marabce ni. 18 In ya yi maka wani laifi ko kuma yana riƙe maka wani
bashi, sai ka mai da shi a kaina. 19 Ni, Bulus, nake rubuta wannan da hannuna. Zan
biya ka, kada ma a yi zancen ranka da kake riƙe mini bashi. 20 Ina fata, ɗan'uwa,
zan sami amfani daga gare ka cikin Ubangiji; ka wartsake zuciyata cikin Kiristi. 21 Da
tabbacin biyayyarka, ina rubuta maka, da sanin za ka yi fiye da abin da na ce.

22 Abu guda ya rage, ka shirya mini masauƙi, domin ina bege za a mayar da ni gare
ku albarkacin addu'o'inku.

23 Efafaras, abokin tarayyata a kurkuku cikin Kiristi Yesu, yana gaishe ka.
24 Haka kuma Markus, Aristarkus, Demas da kuma Luka, abokan aikina.

25 Alherin Ubangiji Yesu Kiristi yă kasance da ruhunku.

* **1:10** Onesimus yana nufin mai amfani.

# Ibraniyawa

1 A dā Allah ya yi wa kakanni-kakanninmu magana ta bakin annabawa a lokuta
dabam-dabam da kuma a hanyoyi iri-iri, 2 amma a waɗannan kwanaki a ƙarshe ya
yi magana da mu ta wurin Ɗansa, wanda ya naɗa magājin dukan abubuwa, wanda
kuma ta wurinsa ya halicci duniya. 3 Ɗan shi ne hasken ɗaukakar Allah, shi ne kuma
ainihin kamanninsa, yana riƙe da dukan abubuwa ta wurin kalmarsa mai iko. Bayan
ya yi tsarkakewa don zunubai, sai ya zauna a hannun daman Maɗaukaki a sama. 4 Ta
haka yake da fifiko a kan mala'iku kamar yadda sunan da ya gāda ya fi nasu fifiko.

*Ɗan ya fi Mala'iku*

5 Gama ga wane daga cikin mala'ikun Allah ya taɓa cewa,
"Kai Ɗana ne;
yau na zama Uba a gare ka"*?
Ko kuwa,
"Zan zama Ubansa,
shi kuma zai zama Ɗana"†?
6 Haka kuma, sa'ad da Allah ya kawo ɗan farinsa a duniya ya ce,
"Bari dukan mala'ikun Allah su yi masa sujada."
7 Da yake magana game da mala'iku kuwa ya ce,
"Ya mai da mala'ikunsa iska,
bayinsa kuma harsunan wuta."‡
8 Amma game da Ɗan ya ce,
"Kursiyinka, ya Allah, zai kasance har abada abadin,
adalci kuma zai zama sandan mulkinka.
9 Ka ƙaunaci abin da yake daidai, ka kuma ƙi mugunta;
saboda haka Allah, Allahnka, ya ɗora ka a bisan abokan zamanka,
ta wurin shafan da ya yi maka da man farin ciki."§
10 Ya kuma ce,
"Tun da farko, ya Ubangiji, ka kafa tushen duniya,
sammai kuma aikin hannuwanka ne.
11 Su za su hallaka, amma kai kana nan;
dukansu za su tsufa kamar riga.
12 Za ka naɗe su kamar mayafi,
kamar riga za su sauya.
Amma kai ba za ka canja ba,
shekarunka kuma ba za su taɓa ƙarewa ba."*
13 Ga wane daga cikin mala'iku Allah ya taɓa cewa,
"Zauna a hannun damana,
sai na sa abokan gābanka
su zama matashin sawunka"†?
14 Ashe, dukan mala'iku ba ruhohi masu hidima ba ne da aka aika don su yi wa
waɗanda za su gāji ceto hidima?

## 2

*Gargaɗi don a mai da hankali*

---

* 1:5 Zab 2.7 † 1:5 2Sam 7.14; 1Tar 17.13 ‡ 1:7 Zab 104.4 § 1:9 Zab 45.6,7 * 1:12 Zab 102.25-27
† 1:13 Zab 110.1

1 Dole mu ƙara mai da hankali sosai ga abubuwan da muka ji, don kada mu kauce.
2 Gama in saƙon da aka faɗi ta bakin mala'iku ya zama tabbatacce, kuma kowane
ƙeta umarni da rashin biyayya suka karɓi sakamakonsu da ya dace, 3 yaya za mu
tsira in muka ƙyale irin wannan babban ceto? Wannan ceto, wanda Ubangiji ne
ya fara sanar, aka kuma tabbatar mana ta bakin waɗanda suka ji shi. 4 Allah shi
ma ya shaida ta wurin alamu, abubuwan banmamaki da mu'ujizai iri-iri, da kuma
baye-bayen Ruhu Mai Tsarki da aka rarraba bisa ga nufinsa.

*An yi Yesu kamar 'yan'uwansa*

5 Ba ga mala'iku ba ne ya sa su yi mulkin duniya mai zuwa, wanda muke magana
a kai ba. 6 Amma akwai wani wurin da wani ya shaida cewa,
"Mene ne mutum, da kake tuna da shi,
ɗan mutum da kake kula da shi?
7 Ka sa shi ƙasa kaɗan da darajar mala'iku;
ka naɗa shi da ɗaukaka da girma,
8 ka kuma sa kome a ƙarƙashin ƙafafunsa."*
Ta wurin sa kome a ƙarƙashinsa, Allah bai bar wani abu da bai sa a ƙarƙashinsa ba.
Duk da haka a yanzu ba mu ga kowane abu a ƙarƙashinsa ba. 9 Sai dai muna ganin
Yesu, wanda aka mai da shi ƙasa kaɗan da darajar mala'iku, yanzu kuwa an naɗa
shi da ɗaukaka da girma domin yă sha wahalar mutuwa, domin ta wurin alherin
Allah yă ɗanɗana mutuwa saboda kowa.
10 Ta wurin kawo 'ya'ya masu yawa zuwa ga ɗaukaka, ya dace cewa Allah, wanda
dominsa da kuma ta wurinsa ne kome yake kasancewa, ya sa tushen cetonsu yă zama
cikakke ta wurin shan wahala. 11 Da shi wanda yake tsarkake mutane da kuma su
waɗanda ake tsarkakewa duk 'yan iyali ɗaya ne. Saboda haka Yesu ba ya kunyan
kiransu 'yan'uwansa. 12 Ya ce,
"Zan sanar da sunanka ga 'yan'uwana;
a gaban jama'a zan rera yabonka."†
13 Har wa yau ya ce,
"Zan dogara gare shi."‡
Ya kuma ce,
"Ga ni, da 'ya'yan da Allah ya ba ni."§
14 Da yake 'ya'yan suna da nama da jini, shi ma sai ya ɗauki kamanninsu na mutum
domin ta wurin mutuwarsa yă hallaka wanda yake riƙe da ikon mutuwa, wato, Iblis
15 ya kuma 'yantar da waɗanda dukan rayuwarsu tsoron mutuwa ya riƙe su cikin
bauta. 16 Gama tabbatacce ba mala'iku ne ya taimaka ba, sai dai zuriyar Ibrahim.
17 Saboda wannan dole a mai da shi kamar 'yan'uwansa ta kowace hanya, domin yă
zama babban firist mai aminci da mai jinƙai cikin hidima ga Allah, yă kuma miƙa
hadayar sulhu saboda zunuban mutane. 18 Domin shi kansa ya sha wahala sa'ad da
aka gwada shi, yana iya taimakon waɗanda ake yi wa gwaji.

# 3

*Yesu ya fi Musa*

1 Saboda haka, 'yan'uwa tsarkaka, waɗanda suke da rabo a kiran nan na sama,
ku kafa tunaninku a kan Yesu, manzo da kuma babban firist wanda muke shaidawa.
2 Ya yi aminci ga wanda ya naɗa shi, kamar yadda Musa ya yi aminci ga dukan gidan
Allah. 3 An ga Yesu ya cancanci girma fiye da Musa, kamar yadda mai ginin gida ya fi
gidan daraja. 4 Gama kowane gida yana da wanda ya gina shi, amma maginin dukan
abu Allah ne. 5 Musa ya yi aminci a matsayin bawa cikin dukan gidan Allah, yana

* **2:8** Zab 8.4-6 † **2:12** Zab 22.22 ‡ **2:13** Ish 8.17 § **2:13** Ish 8.18

ba da shaida a kan abubuwan da za a faɗa nan gaba. [6] Amma Kiristi mai aminci ne
kamar ɗa a gidan Allah. Mu kuwa gidansa ne, in muka tsaya gabanmu gadi da kuma
begen da muke taƙama a kai.

### *Gargaɗi a kan rashin bangaskiya*

[7] Kamar dai yadda Ruhu Mai Tsarki ya ce,
"Yau, in kuka ji muryarsa,
[8] kada ku taurare zukatanku,
yadda kuka yi a tawayen nan,
a lokacin gwaji a hamada,
[9] inda kakanninku suka gwada ni, suka kuma gwada ni,
ko da yake a cikin shekaru arba'in sun ga abin da na yi.
[10] Shi ya sa na yi fushi da wancan zamani,
na kuma ce, 'Kullum zukatansu a karkace suke,
ba su kuma san hanyoyina ba.'
[11] Saboda haka na yi rantsuwa a cikin fushina,
'Ba za su taɓa shiga hutuna ba.' "*
[12] Ku lura fa, 'yan'uwa, cewa kada waninku yă kasance da zuciya mai zunubi marar
bangaskiya da takan juye daga bin Allah mai rai. [13] Sai dai ku ƙarfafa juna kullum,
muddin akwai lokacin da ana ce da shi Yau, don kada waninku yă zama mai taurin
zuciya ta wurin ruɗun zunubi. [14] Mu masu tarayya ne da Kiristi idan mun riƙe
bangaskiyarmu da ƙarfi daga farko har zuwa ƙarshe. [15] Kamar yadda aka faɗa cewa,
"Yau, in kuka ji muryarsa,
kada ku taurare zukatanku
kamar yadda kuka yi a tawayen nan."†
[16] Su wane ne suka ji suka kuma yi tawaye? Ba su ne duk waɗanda Musa ya bi da
su daga Masar ba? [17] Da su wane ne kuwa ya yi fushi har shekaru arba'in? Ba da
waɗanda suka yi zunubi, waɗanda suka mutu a hamada ba? [18] Kuma ga su wane ne
Allah ya rantse cewa ba za su taɓa shiga hutunsa ba, in ba ga marasa biyayyan nan
ba? [19] Saboda haka mun ga cewa ba su iya shiga ba, saboda rashin bangaskiyarsu
ne.

# 4

### *Hutun Asabbaci don mutanen Allah*

[1] Saboda haka, da yake alkawarin shiga hutunsa yana nan har yanzu, sai mu yi
hankali kada waninku yă kāsa shiga. [2] Gama mu ma mun ji an yi mana wa'azin
bishara, kamar yadda su ma suka ji; sai dai saƙon da suka ji ba tă amfane su ba,
domin waɗanda suka ji ba su karɓe shi da bangaskiya ba. [3] Mu kam da muka gaskata
mu ne muka shiga wannan hutu, kamar yadda Allah ya ce,
"Saboda haka na yi rantsuwa cikin fushina,
'Ba za su taɓa shiga hutuna ba.' "*
Allah ya faɗa haka ko da yake ya riga ya kammala aikinsa tun halittar duniya. [4] Gama
a wani wuri ya yi magana a kan rana ta bakwai cikin waɗannan kalmomi, "A rana
ta bakwai kuwa Allah ya huta daga dukan aikinsa."† [5] Haka kuma a nassin nan ya
ce, "Ba za su taɓa shiga hutuna ba."
[6] Har yanzu dai da sauran dama domin waɗansu su shiga, su kuwa waɗanda aka
fara yi wa albishirin nan sun kāsa shiga saboda rashin biyayya. [7] Saboda haka Allah
ya sāke sa wata rana, yana kiranta Yau, bayan wani dogon lokaci Allah ya yi magana
ta bakin Dawuda, yadda aka riga aka faɗa,

* **3:11** Zab 95.7-11 † **3:15** Zab 95.7,8 * **4:3** Zab 95.11; haka ma a aya 5 † **4:4** Far 2.2

“Yau, in kuka ji muryarsa,
kada ku taurare zukatanku.”‡
8 Gama da a ce Yoshuwa ya ba su hutu, da Allah bai yi magana daga baya a kan
wata rana dabam ba. 9 Har yanzu, akwai wani hutun Asabbacin da ya rage domin
mutanen Allah; 10 gama duk wanda ya shiga hutun Allah, shi ma yakan huta daga
nasa aiki, kamar yadda Allah ya huta daga nasa. 11 Saboda haka, bari mu yi iyakacin
ƙoƙarinmu mu shiga wannan hutu, don kada wani yă kāsa ta wurin bin gurbinsu na
rashin biyayya.
12 Maganar Allah tana da rai, tana kuma da ƙarfin aiki. Ta fi kowane takobi mai
baki biyu kaifi. Maganarsa takan ratsa har ciki-ciki, tana raba rai da ruhu, gaɓoɓi
da kuma ɓargon ƙashi; har sai ta tone ainihi wane ne muke. 13 Babu wani abu cikin
dukan halittar da yake ɓoye daga fuskar Allah. Kowane abu a buɗe yake yana kuma
a shimfiɗe a idanun wanda dole mu ba da lissafi a gare shi.

*Yesu babban firist mai girma*

14 Saboda haka, da yake muna da babban firist mai girma wanda ya ratsa sama,
Yesu Ɗan Allah, bari mu riƙe bangaskiyan nan wadda muke shaidawa da ƙarfi.
15 Gama babban firist da muke da shi ba marar juyayin kāsawarmu ba ne, amma
muna da wanda aka gwada ta kowace hanya, kamar dai yadda akan yi mana, duk
da haka bai yi zunubi ba. 16 Saboda haka sai mu matso kusa da kursiyin alheri da
ƙarfi zuciya, don mu sami jinƙai mu kuma sami alherin da zai taimake mu a lokacin
bukata.

# 5

1 Akan zaɓi kowane babban firist daga cikin mutane ne, akan kuma naɗa shi domin
yă wakilce su a kan al’amuran Allah, domin yă miƙa kyautai da hadayu saboda
zunubai. 2 Da yake babban firist ɗin mai kāsawa ne, yana iya bin da jahilai da
kuma waɗanda suka kauce hanya, a hankali. 3 Shi ya sa dole yă miƙa hadayu domin
zunubansa, da kuma domin zunuban mutane.
4 Ba wanda yakan kai kansa a wannan matsayi mai girma; sai ko Allah ya kira shi,
kamar yadda aka yi wa Haruna. 5 Haka ma Kiristi bai kai kansa neman ɗaukaka na
zama babban firist ba. Allah ne dai ya ce masa,
“Kai Ɗana ne;
yau na zama Uba a gare ka.”*
6 Ya kuma ya ce a wani wuri,
“Kai firist ne na har abada,
bisa ga tsarin Melkizedek.”†
7 A lokacin da Yesu ya yi rayuwa a duniya, ya yi addu’o’i da roƙe-roƙe tare da kuka
mai zafi da kuma hawaye ga wannan wanda yake da ikon cetonsa daga mutuwa, aka
kuwa ji shi saboda tsananin bangirman da ya yi. 8 Ko da yake shi ɗa ne, ya yi biyayya
ta wurin shan wahala 9 kuma da aka mai da shi cikakke, sai ya zama hanyar samun
madawwamin ceto ga dukan waɗanda suke masa biyayya. 10 Allah kuwa ya naɗa
shi yă zama babban firist, bisa ga tsarin Melkizedek.

*Gargaɗi game da kaucewa*

11 Muna da abubuwa masu yawa da za mu faɗa game da wannan batu, sai dai yana
da wuya a bayyana, da yake ba ku da saurin ganewa. 12 Gaskiya, a yanzu ya kamata
a ce kun zama malamai, sai ga shi kuna bukatar wani yă sāke koya muku abubuwa
masu sauƙi game da abin da Allah ya faɗa. Kuna bukatar madara, ba abinci mai
kauri ba! 13 Duk wanda yake rayuwa a kan madara, shi kamar jariri ne har yanzu,

‡ **4:7** Zab 95.7,8 * **5:5** Zab 2.7 † **5:6** Zab 110.4

kuma bai san ainihi mene ne ya dace ba. 14 Amma abinci mai kauri na balagaggu ne,
waɗanda suka hori kansu don su bambanta tsakanin nagarta da mugunta.

# 6

1 Dole mu yi ƙoƙarin zama balagaggu mu kuma fara tunani game da abubuwan da
suka fi koyarwan nan mai sauƙi game da Kiristi. Bai kamata mu ci gaba da magana
game da me ya sa dole mu juye daga ayyukan da suke kawo mutuwa da kuma me
ya sa za mu kasance da bangaskiya a cikin Allah ba. 2 Kuma bai kamata mu ci gaba
da koyar da umarnai game da baftisma, ɗibiya hannuwa, tashin matattu, da kuma
madawwamin hukunci ba. 3 Da yardar Allah, za mu ci gaba ga ƙarin ganewa.
4 Waɗanda suka taɓa samun haske, waɗanda suka ɗanɗana kyauta ta sama,
waɗanda suka sami rabo cikin Ruhu Mai Tsarki, 5 waɗanda suka ɗanɗana daɗin
maganar Allah da kuma ikokin zamani mai zuwa, 6 ba ya yiwuwa a sāke kawo su ga
tuba in suka kauce, domin suna sāke gicciye Ɗan Allah ke nan suna kuma kunyata
shi a gaban jama'a. 7 Kasar da take shan ruwan sama da yake fāɗi a kanta kullum
da kuma take ba da hatsin da yake da amfani ga waɗanda ake noma dominsu, takan
sami albarkar Allah. 8 Amma ƙasar da take ba da ƙaya da sarƙaƙƙiya ba ta da amfani
tana kuma cikin hatsarin la'ana. A ƙarshe za a ƙone ta.
9 Abokaina, ko da yake muna irin maganan nan, mun tabbata kuna yi abubuwan
nan masu kyau da waɗanda suka sami ceto suke yi. 10 Allah ba marar adalci ba
ne. Ba zai manta da aikinku da kuma ƙaunar da kuka nuna masa wajen taimakon
mutanensa da kuma ci gaba da taimakonsu da kuke yi ba. 11 Muna so kowannenku
yǎ nuna ƙwazon nan har zuwa ƙarshe, domin ku tabbatar da begenku. 12 Ba ma so
ku zama masu ƙyuya, sai dai ku yi koyi da waɗanda ta wurin bangaskiya da haƙuri
suka gāji abin da aka yi alkawari.

### *Alkawarin Allah tabbatacce ne*

13 Babu wanda ya fi Allah, saboda haka sa'ad da ya yi alkawari ga Ibrahim, sai ya
rantse da sunansa, 14 cewa, "Tabbatacce zan albarkace ka in kuma ba ka zuriya mai
yawa."* 15 Haka kuwa bayan Ibrahim ya jira da haƙuri, sai ya karɓi abin da aka yi
alkawari.
16 In mutane za su yi rantsuwa sukan yi haka da wanda ya fi su ne, rantsuwar
kuwa takan tabbatar da abin da aka faɗa ta kuma kawo ƙarshen dukan gardama.
17 Saboda haka da Allah ya so yǎ bayyana nufinsa marar canjawa a sarari ga magādan
abin da aka yi alkawari, sai ya tabbatar da shi da rantsuwa. 18 Allah ba ya karya!
Haka ma alkawuransa da rantsuwarsa abubuwa biyu ne da ba a iya canjawa. Mun
gudu zuwa wurin Allah domin kāriya. Ya kamata alkawuransa su ƙarfafawa sosai
mu riƙe begen nan da yake gabanmu. 19 Muna da wannan bege kamar anka na rai,
kafaffe da kuma tabbatacce. Yana shiga tsattsarkan wuri na can ciki a bayan labule,
20 inda Yesu, wanda ya sha gabanmu, ya shiga a madadinmu. Ya zama babban firist
na har abada, bisa ga tsarin Melkizedek.

# 7

### *Melkizedek firist*

1 Wannan Melkizedek sarkin Salem ne da kuma firist na Allah Mafi Ɗaukaka. Shi
ne ya sadu da Ibrahim ya albarkace shi sa'ad da Ibrahim ya dawowa daga cin nasara
a bisa sarakuna, 2 Ibrahim kuwa ya ba shi kashi ɗaya bisa goma na kome. Ma'anar
sunan Melkizedek ita ce, "sarkin adalci." Amma da yake Salem yana nufin "salama,"
shi kuma "Sarkin salama" ne. 3 Ba shi da mahaifi ko mahaifiya, ba shi da asali, ba
shi da farko ko ƙarshe, shi dai kamar Ɗan Allah ne kuma firist ne har abada.

* **6:14** Far 22.17

[4] Ku dubi irin girman da Melkizedek mana. Ko kakanmu Ibrahim ma ya ba shi kashi
ɗaya bisa goma na ganima! [5] Yanzu doka ta umarci zuriyar Lawi waɗanda suka zama
firistoci su karɓi kashi ɗaya bisa goma daga wurin mutane, wato, ʼyanʼuwansu, ko
da yake ʼyanʼuwansu zuriyar Ibrahim ne. [6] Ko da yake Melkizedek ba daga zuriyar
Lawi ba ne, duk da haka Ibrahim ya ba shi kashi ɗaya bisa goma na abin da yake
da shi, Melkizedek kuwa ya sa masa albarka, shi da aka yi wa alkawura. [7] Kowa ya
sani cewa na gaba shi yake sa wa na baya albarka. [8] Firistoci ake ba wa kashi ɗaya
bisa goma na abin da mutane suke samu. Amma dukan firistoci sukan mutu, sai
dai Melkizedek, kuma nassi ya ce yana da rai. [9] Ana ma iya cewa zuriyar Lawi, mai
karɓar kashi ɗaya bisa goma daga mutane, ya ba da kashi ɗaya bisa goma ta wurin
Ibrahim, [10] wannan ya kasance haka domin an haifi Lawi daga baya a iyalin Ibrahim
wanda ya ba wa Melkizedek kashi ɗaya bisa goma.

*Yesu kamar Melkizedek ne*

[11] Ko da yake Dokar Musa ta ce dole firistoci su kasance zuriyar Lawi, waɗannan
firistoci ba su iya sa wani yă zama cikakke ba. Saboda akwai bukata wani firist kamar
Melkizedek ya zo, a maimakon wani daga iyalin Haruna. [12] Gama in aka canja yadda
ake zaɓan firist, dole a canja Dokar ita ma. [13] Mutumin da muke wannan zance a
kai, ai, shi na wata kabila ce dabam, wadda ba wani daga kabilar da ya taɓa yin
hidima a bagade. [14] Kowa ya san cewa Ubangijinmu ya fito ne daga zuriyar Yahuda
ne, kuma Musa bai taɓa ce firistoci za su fito daga wannan kabila ba. [15] Canjin nan a
Dokar Allah ya ƙara fitowa fili da wani firist dabam wanda yake kamar Melkizedek
ya bayyana. [16] Ya zama firist ne ba saboda ya cika wata ƙaʼida ta zama zuriyar Lawi
ba, sai dai bisa ga ikon ran da ba a iya hallakawa. [17] Gama nassi ya ce,

“Kai firist ne na har abada,
bisa ga tsarin Melkizedek.”*

[18] Ta haka aka kawar da ƙaʼida marar ƙarfi da kuma marar amfani [19] (gama doka
ba tă mai da wani abu cikakke ba), yanzu kuwa bege mafi kyau ya ɗauki matsayinta.
Ta haka kuma muka matso kusa da Allah.

[20] Ba kuwa da rashin rantsuwa aka yi haka ba. Waɗansu sun zama firistocin ba
tare da wata rantsuwa ba, [21] shi wannan ya zama firist ta wurin rantsuwar da Allah
ya yi da ya ce masa,

“Ubangiji ya rantse,
ba kuwa zai canja zuciyarsa ba,
‘Kai firist ne na har abada.’ ”†

[22] Saboda wannan rantsuwa, Yesu ya zama tabbacin alkawari mafi kyau.

[23] To, akwai waɗannan firistoci da yawa, da yake mutuwa ta hana su cin gaba da
aikin zaman firist; [24] amma Yesu ba zai mutu ba, don haka zai zama firist har abada.
[25] Saboda haka ya iya ba da ceto gaba ɗaya ga masu zuwa wurin Allah ta wurinsa,
gama kullum a raye yake saboda yă yi roƙo dominsu.

[26] Irin wannan babban firist ne muke bukata, shi mai tsarki ne, marar aibi, mai
tsabta, ba kamar mu masu zunubi ba sam. An ɗaukaka shi fiye da kome a sama. [27] Ba
ya bukata yă yi ta miƙa hadayu kowace rana saboda zunubansa, saʼan nan saboda
zunuban mutane kamar sauran firistoci. Ya miƙa hadaya sau ɗaya tak, saʼad da ya
miƙa kansa. [28] Gama doka takan naɗa babban firist a cikin mutane masu kāsawa;
amma rantsuwar da ta zo bayan dokar, ta naɗa Ɗan, wanda aka mai da shi cikakke
har abada.

# 8

*Babban firist na sabuwar yarjejjeniya*

* **7:17** Zab 110.4 † **7:21** Zab 110.4

1 Abin da muke magana a nan shi ne, muna da irin wannan babban firist, wanda
ya zauna a hannun dama na kursiyin Maɗaukaki a sama, 2 wanda yake hidima a
cikin wuri mai tsarki, tabanakul na gaskiya wanda Ubangiji ne ya kafa, ba mutum
ba.
3 Da yake dole kowane babban firist da aka naɗa yă miƙa baye-baye da hadayu,
haka ma wannan ya bukaci yă kasance da abin da zai miƙa. 4 Da a ce yana a duniya
ne, da bai zama firist ba, domin a nan akwai mutanen da doka ta naɗa don su miƙa
baye-baye. 5 Suna hidima a cikin tsattsarkan wuri wanda yake hoto da kuma siffar
abin da yake cikin sama. Shi ya sa aka gargaɗi Musa sa'ad da yana dab da gina
tabanakul cewa, "Ka lura fa, ka yi kome daidai bisa ga zānen da aka nuna maka a
kan dutsen."[*] 6 Amma hidimar da Yesu ya karɓa tana da fifiko a kan tasu, kamar
yadda alkawarin da shi ne yake matsakanci ya fi na dā fifiko nesa, an kuma kafa shi
a kan alkawura mafi kyau.
7 Gama da a ce alkawari na fari ba shi da wani laifi, da ba sai an sāke neman wani
ba. 8 Amma Allah ya sami mutane da laifi[†] ya ce,
"Ina gaya muku lokaci yana zuwa,
sa'ad da zan yi sabon alkawari
da gidan Isra'ila
da kuma gidan Yahuda.
9 Ba zai zama kamar irin alkawarin
da na yi da kakanni-kakanninsu
sa'ad da na kama hannunsu
don in fitar da su daga Masar ba,
domin ba su yi aminci da alkawarina ba,
sai na juya musu baya,
in ji Ubangiji.
10 Wannan shi ne alkawarin da zan yi da gidan Isra'ila,
bayan lokacin nan,
in ji Ubangiji.
Zan sa dokokina a cikin zukatansu,
in kuma rubuta su a kan zukatansu.
Zan zama Allahnsu,
su kuwa za su zama mutanena.
11 Mutum ba zai ƙara koya wa maƙwabcinsa ba,
balle mutum yă ce wa ɗan'uwansa, 'Ka san Ubangiji,'
domin dukansu za su san ni,
daga ƙaraminsu zuwa babba.
12 Gama zan gafarta muguntarsu
ba zan kuma ƙara tuna da zunubansu ba."[‡]
13 Ta wurin kira wannan alkawari "sabo," ya mai da na farin tsoho ke nan; abin
da yake tsoho yana kuma daɗa tsufa, zai shuɗe nan ba da daɗewa ba.

# 9

*Sujada a cikin tabanakul na duniya*
1 Alkawarin farko ya ƙunshi ƙa'idodi don sujada da kuma tsattsarkan wuri a
duniya. 2 An kafa tabanakul. A cikin ɗakinsa na farko akwai wurin ajiye fitila, tebur
da kuma keɓaɓɓen burodi; an kira wannan Wuri Mai Tsarki. 3 Sa'an nan akwai
labule, kuma a bayan labulen akwai ɗaki na biyu da ake kira Wuri Mafi Tsarki,
4 wanda yake da bagaden zinariya na turare da kuma akwatin alkawarin da aka

---
[*] **8:5** Fit 25.40 [†] **8:8** Za a fassara waɗansu rubuce-rubucen hannu na dā laifi ya kuma ce wa mutane. [‡] **8:12** Irm 31.31-34

dalaye da zinariya. A cikin akwatin alkawarin akwai tulun zinariya mai Manna a
ciki, sandan Haruna wanda ya yi toho, da kuma allunan dutsen alkawari. 5 A bisa
akwatin alkawarin kuwa akwai kerubobi na Ɗaukaka, waɗanda suka inuwantar da
murfin kafara da fikafikansu.* Sai dai ba za mu tattauna waɗannan abubuwa dalla-dalla a yanzu ba.

6 Sa'ad da aka shirya kome haka, sai firistoci suka shiga kullum cikin ɗaki na waje
don su yi hidimarsu. 7 Amma babban firist ne kaɗai yakan shiga ɗaki na ciki-ciki,
sau ɗaya tak a shekara, kuma sai da jini, wanda yakan miƙa domin zunubansa da
kuma domin zunuban da mutane suka yi a cikin rashin sani. 8 Ta haka Ruhu Mai
Tsarki ya nuna cewa ba a riga an bayyana hanyar shiga Wuri Mafi Tsarki ba tukuna,
muddin tabanakul na fari yana nan tsaye. 9 Wannan ma yana da ma'ana wa mutane
a yau. Ya nuna cewa ba za mu iya wanke lamirinmu ta wurin miƙa baye-baye da
hadayu ba. 10 Waɗannan ƙa'idodi sun shafi sha'anin abinci da abin sha ne kawai da
kuma ƙa'idodi tsarkake kanmu. Dokoki game da abubuwa na waje da ake amfani da
su za su kasance ne sai lokacin ya yi da za a kawo abu mafi kyau.

### *Jinin Kiristi*

11 Sa'ad da Kiristi ya zo a matsayin babban firist na kyawawan abubuwan da suka
riga suka kasance a nan, ya bi ta cikin tabanakul mafi girma da kuma mafi cikakke
wanda ba mutum ne ya yi ba, wato, ba na wannan halitta ba. 12 Bai shiga ta wurin
jinin awaki da na maruƙa ba; amma ya shiga Wuri Mafi Tsarki sau ɗaya tak ta
wurin jininsa, bayan ya samo madawwamiyar fansa. 13 In har akan yayyafa jinin
awaki da na bijimai da kuma tokar karsanar a kan waɗanda suke marasa tsabta
bisa ga al'ada, a tsarkake su yadda za su zama masu tsabta a waje, 14 balle jinin
Kiristi, wanda ta wurin Ruhu madawwami ya miƙa kansa marar aibi ga Allah, ai, zai
tsabtacce lamirinmu daga ayyukan da suke kai ga mutuwa, don mu bauta wa Allah
mai rai!

15 Saboda haka Kiristi shi ne matsakancin sabon alkawari, don waɗanda aka kira
su sami madawwamin gādon da aka yi alkawari, yanzu da ya mutu a matsayin mai
fansa don yă 'yantar da su daga zunuban da aka aikata a ƙarƙashin alkawari na
farko.

16 Sa'ad da wani ya yi alkawari game da gādonsa,† dole a tabbatar da mutuwar
wanda ya yi ta, 17 domin alkawarin gādo yana aiki ne kawai bayan mai yinsa ya
mutu, ba ya taɓa aiki yayinda mai yinsa yana da rai. 18 Shi ya sa alkawari na farko
bai fara aiki ba sai da aka zub da jini. 19 Sa'ad da Musa ya sanar wa dukan mutane
kowane umarni na doka, sai ya ɗauki jinin maruƙa tare da ruwa, jan ulu da kuma
rassan hizzob, ya yayyafa a kan naɗaɗɗen littafin da kuma a kan dukan mutanen.
20 Ya ce, "Wannan shi ne jinin alkawarin da Allah ya umarce ku ku kiyaye."‡ 21 Ta
haka ya yayyafa jinin a kan tabanakul da kuma a kan dukan kayayyakin da ake
amfani da su don yin hidima. 22 Tabbatacce, doka ta bukaci a tsabtacce kusa kowane
abu da jini, kuma in ba tare da zub da jini ba babu gafara.

23 Waɗannan abubuwa hotuna ne kawai na abin da yake a sama, dole kuma a
tsarkake su ta wurin waɗannan ƙa'idodi. Amma dole a tsarkake ainihin abubuwa
na sama da wani abu mafi kyau. 24 Gama Kiristi bai shiga wani wuri tsattsarka da
mutum ya yi ba, wanda yake hoto ne kawai na gaskataccen, a'a sama kanta ya shiga,
domin yă bayyana a gaban zatin Allah a yanzu saboda mu. 25 Bai kuwa shiga sama
domin yă yi ta miƙa kansa a kai a kai, yadda babban firist yake shiga Wuri Mafi
Tsarki kowace shekara da jinin da ba nasa ba. 26 Da a ce haka ne, ai, da Kiristi ya sha
wahala sau da yawa tun halittar duniya. Amma yanzu ya bayyana sau ɗaya tak a

* **9:5** A al'adance mazaunin jinƙai † **9:16** Kalmar Girik guda da alkawari; haka ma a aya 17 ‡ **9:20** Fit 24.8

ƙarshen zamanai domin yǎ kawar da zunubi ta wurin miƙa kansa hadaya. 27 Kamar
dai yadda aka ƙaddara wa mutum yǎ mutu sau ɗaya, bayan haka kuma sai shari'a,
28 haka aka miƙa Kiristi hadaya sau ɗaya domin yǎ ɗauke zunuban mutane masu
yawa; zai kuma bayyana sau na biyu, ba don yǎ ɗauki zunubi ba, sai dai don yǎ
kawo ceto ga waɗanda suke jiransa.

# 10

### *Hadayar Kiristi sau ɗaya tak*

1 Dokar, inuwa ce kawai ta kyawawan abubuwa masu zuwa, wannan inuwar ba
ita ce ainihin abubuwan ba ne. Saboda haka ba za tǎ taɓa mai da masu matsowa
kusa don yin sujada cikakku ta wurin irin hadayun da ake maimaitawa ba fasawa
shekara-shekara ba. 2 Da a ce za tǎ iya, da ba su daina miƙa hadayu ba? Ai, da an
riga an tsabtacce masu yin sujada sau ɗaya tak, da kuma ba za su ƙara damuwa da
zunubansu ba. 3 Amma waɗancan hadayu abin tunawa da zunubai ne na kowace
shekara, 4 domin ba zai taɓa yiwuwa jinin bijimai da na awaki yǎ kawar da zunubai
ba.

5 Saboda haka, sa'ad da Kiristi ya shigo duniya ya ce,

"Hadaya da sadaka kam ba ka so,
sai dai ka tanadar mini jiki;
6 hadayun ƙonawa da kuma hadayun zunubi ba ka ji daɗin.
7 Sai na ce, 'Ga ni nan, a rubuce yake cikin naɗaɗɗen littafi
na zo in aikata nufinka, ya Allah.' "*

8 Da farko ya ce, "Hadayu da sadakoki, hadayun ƙonawa da hadayun zunubi ba ka
so, ba ka kuwa jin daɗinsu" (ko da yake doka ta bukaci a yi su). 9 Sa'an nan ya ce,
"Ga ni nan, na zo in aikata nufinka." Ya kawar da na farkon domin yǎ kafa na biyun.
10 Kuma bisa ga wannan nufi, aka mai da mu masu tsarki ta wurin miƙa hadayar
jikin Yesu Kiristi sau ɗaya tak.

11 Kowace rana kowane firist yakan tsaya yin hidimar ibadarsa; sau da sau yakan
miƙa hadayu iri ɗaya, waɗanda ba za su taɓa kawar da zunubai ba. 12 Amma da
Kiristi ya miƙa hadaya ɗaya ta dukan lokaci saboda zunubai, sai ya zauna a hannun
dama na Allah. 13 Tun daga lokacin nan yana jira a mai da abokan gābansa matashin
ƙafafunsa, 14 gama ta wurin hadayan nan guda ɗaya ya kammala har abada waɗanda
ake tsarkake.

15 Ruhu Mai Tsarki ma ya yi mana shaida game da wannan. Da farko ya ce,

16 "Wannan shi ne alkawarin da zan yi da su
bayan wannan lokaci,
in ji Ubangiji.
Zan sa dokokina a cikin zukatansu,
in kuma rubuta su a kan zukatansu."†
17 Sai ya ƙara da cewa,
"Zunubansu da kurakuransu
ba zan ƙara tunawa da su ba."‡
18 In an gafarta zunubai, babu sauran bukatar miƙa hadaya.

### *Kira don a adana bangaskiya*

19 Saboda haka, 'yan'uwa, da yake muna da wannan tabbaci na shiga Wuri Mafi
Tsarki ta wurin jinin Yesu, 20 ta wurin sabuwa, rayayyiyar hanya kuma wadda aka
buɗe mana ta labulen nan, wato, jikinsa, 21 da yake kuma muna da babban firist mai
mulkin gidan Allah, 22 bari mu matso kusa da Allah da zuciya mai gaskiya da kuma
cikakken tabbaci mai zuwa ta wurin bangaskiya. Bari mu bar zukatan da tsabta,

* **10:7** Zab 40.6-8 (dubi Seftuwajin) † **10:16** Irm 31.33 ‡ **10:17** Irm 31.34

lamirinmu babu mugunta, da kuma jikunanmu a wanke da ruwa. 23 Bari mu tsaya
da ƙarfi a kan ga begen da muka ce namu ne, gama shi da ya yi alkawarin, mai
aminci ne. 24 Bari kuma mu yi tunani a kan yadda za mu gargaɗe juna ga ƙauna da
kuma ayyuka nagari. 25 Kada mu daina taruwa kamar yadda waɗansu suka saba, sai
dai mu ƙarfafa juna, tun ba ma da kuka ga Ranan nan tana kusatowa ba.

26 Ba wata hadayar da za a yi don mutanen da suka yanke shawara su yi ci gaba
da yin zunubi da gangan bayan sun sami sanin gaskiya. 27 A maimakon haka za
su kasance da babban fargabar hukunci da kuma ta ƙunar wuta wadda za tă cinye
abokan gāban Allah. 28 Duk wanda ya ƙi ya kiyaye dokar Musa akan kashe shi ba
tausayi, a kan shaidar mutum biyu ko uku. 29 Wane irin hukunci mai tsanani ne kuke
tsammani zai dace da mutumin da ya nuna rashin bangirma ga Ɗan Allah, wanda ya
yi banza da jinin nan na alkawarin da ya tsarkake shi, wanda kuma ya zargi Ruhun
alheri? 30 Gama mun san shi, wannan wanda ya ce, "Ramuwa tawa ce; zan rama,"§
da kuma, "Ubangiji zai yi wa mutanensa hukunci."* 31 Abu mai matuƙar bantsoro
ne a fāɗa cikin hannuwan Allah mai rai.

32 Ku tuna da kwanakin nan da suka wuce bayan kun sami haske, sa'ad da kuka
tsaya daram a tsananin shan wahala. 33 Wani lokaci a fili an tsananta muku aka kuma
zage ku aka kuma tsananta muku; a wani lokaci kuma kuka tsaya tare da waɗanda
aka yi musu haka. 34 Kuka ji tausayin waɗanda suke cikin kurkuku, da farin ciki
kuma kuka yarda ku rabu da dukiyar da aka ƙwace muku, domin ku kanku kun san
cewa kuna da madawwamiyar dukiya mafi kyau. 35 Saboda haka kada ku yar da
tabbacinku; za a sāka muku a yalwace.

36 Kuna bukata ku jimre don sa'ad da kuka aikata nufin Allah, za ku karɓi abin da
ya yi alkawari. 37 Gama,

"A cikin ɗan lokaci kaɗan,
mai zuwan nan zai zo
ba kuwa zai yi jinkiri ba.

38 Amma,

"Mai adalcina zai rayu ta wurin bangaskiya.
In kuwa ya ja da baya,
ba zan ji daɗinsa ba."†

39 Amma mu ba na waɗanda suke ja da baya, su kuma hallaka ba ne, amma na
waɗanda suka gaskata, suka kuma sami ceto ne.

# 11

*Ta wurin bangaskiya*

1 Bangaskiya ita ce kasance tabbacin abin da muke bege a kai da kuma tabbatar da
abin da ba mu gani ba. 2 Abin da aka yabi kakanni na dā a kai ke nan.

3 Ta wurin bangaskiya ne muka fahimci cewa an halicci duniya bisa ga umarnin
Allah, saboda an halicce abin da ake gani daga abin da ba a gani.

4 Ta wurin bangaskiya Habila ya miƙa wa Allah hadayar da ta fi wadda Kayinu ya
miƙa. Ta wurin bangaskiya aka yabe shi cewa shi mai adalci ne, sa'ad da Allah ya yi
magana mai kyau game da bayarwarsa. Ta wurin bangaskiya kuma har yanzu yana
magana, ko da yake ya riga ya mutu.

5 Ta wurin bangaskiya ne aka ɗauki Enok daga wannan rayuwa, ta haka bai
ɗanɗana mutuwa ba; ba a kuwa same shi ba, domin Allah ya ɗauke shi. Gama kafin
a ɗauke shi, an yabe shi a kan ya gamshi Allah. 6 In ba tare da bangaskiya ba kuwa,

§ **10:30** M Sh 32.35 * **10:30** M Sh 32.36; Zab 135.14 † **10:38** Hab 2.3,4

ba ya yiwuwa a gamshi Allah, domin duk mai zuwa wurin Allah dole yă gaskata cewa yana nan, kuma shi ne yakan sāka wa waɗanda suke nemansa da gaske.

7 Ta wurin bangaskiya Nuhu, sa'ad da aka yi masa gargaɗi a kan abubuwan da ba a gani ba tukuna, a cikin tsoro mai tsarki ya sassaƙa jirgi don ceton iyalinsa. Ta wurin bangaskiyarsa ya hukunta duniya ya kuma zama magājin adalcin da ake samu ta wurin bangaskiya.

8 Ta wurin bangaskiya ne Ibrahim, sa'ad da aka kira shi ya fita zuwa wata ƙasar da zai karɓi gādo daga baya, ya kuwa yi biyayya ya tafi, ko da yake bai san inda
za shi ba. 9 Ta wurin bangaskiya ya yi zama a ƙasar da aka yi masa alkawari
kamar baƙo a baƙuwar ƙasa; ya zauna a tentuna, haka ma Ishaku da Yaƙub,
waɗanda su ma magādan alkawarin nan ne tare da shi. 10 Gama yana zuba ido
ga birnin nan mai tushe, wanda mai zānen gininsa da kuma mai gininsa Allah ne.
11 Ta wurin bangaskiya Ibrahim, ko da yake shekarunsa sun wuce, Saratu kanta
kuma bakararriya ce ya iya zama mahaifi domin ya* amince cewa shi wanda ya
yi alkawarin mai aminci ne. 12 Saboda haka, daga mutum ɗaya, wanda dā shi ma da
matacce kusan ɗaya ne, zuriya masu yawa suka fito kamar taurari a sararin sama da kuma kamar yashin da ba a iya ƙirgawa a bakin teku.

13 Duk mutanen nan suna cikin bangaskiya sa'ad da suka mutu. Ba su kuwa karɓi abubuwan da aka yi alkawari ba; sun dai hango su suka kuma marabce su daga
nesa. Suka kuma amince cewa su baƙi ne, bare kuma a duniya. 14 Mutane masu
faɗin irin abubuwan nan sun nuna cewa suna neman ƙasar da take tasu. 15 Da a ce
suna tunanin ƙasar da suka bari a baya, da sun riga sun sami damar komawa. 16 A
maimako, suna marmarin wata ƙasa mafi kyau, ta sama. Saboda haka Allah ba ya kunya a kira shi Allahnsu, domin ya riga ya shirya musu birni.

17 Ta wurin bangaskiya Ibrahim, sa'ad da Allah ya gwada shi, sai ya miƙa Ishaku
hadaya. Shi da ya karɓi alkawaran ya yi shirin miƙa makaɗaicin ɗansa, 18 ko da
yake Allah ya ce masa, "Ta wurin Ishaku ne za a lissafta zuriyarka."† 19 Ibrahim ya
yi tunani cewa Allah yana iya tā da matattu, a misalce kuwa, ya sāke karɓan Ishaku daga matattu.

20 Ta wurin bangaskiya ne Ishaku ya albarkaci Yaƙub da Isuwa game da nan gabansu.

21 Ta wurin bangaskiya ne Yaƙub, sa'ad da yake bakin mutuwa, ya albarkaci kowane ɗan Yusuf, ya kuma yi sujada yayinda yake jingine a kan sandansa.

22 Ta wurin bangaskiya ne Yusuf, sa'ad da kwanakinsa suka yi kusan ƙarewa, ya yi magana game da fitowar Isra'ilawa daga Masar ya kuma ba da umarni game da ƙasusuwansa.

23 Ta wurin bangaskiya ne iyayen Musa suka ɓoye shi har wata uku bayan haihuwarsa, domin sun ga cewa shi ba kamar sauran yara ba ne, ba su kuwa ji tsoron umarnin sarki ba.

24 Ta wurin bangaskiya ne Musa, sa'ad da ya yi girma, ya ƙi a kira shi ɗan diyar
Fir'auna. 25 Ya zaɓa yă sha wahala tare da mutanen Allah, maimakon yă ji daɗin
sha'awace-sha'awacen zunubi na ɗan lokaci. 26 Ya ɗauki wulaƙancin da yake sha
saboda Kiristi ya fi dukiyar Masar daraja, domin ya sa ido ga ladansa. 27 Ta wurin
bangaskiya ya bar Masar, ba tare da jin tsoron fushin sarki ba; ya kuwa jure domin
ya ga wannan wanda ba a iya gani. 28 Ta wurin bangaskiya ya kiyaye Bikin Ketarewa
ya kuma yayyafa jini, domin kada mai hallakar 'ya'yan fari yă taɓa 'ya'yan fari na Isra'ila.

---

* **11:11** Ko kuwa Ta wurin bangaskiya Saratu ma, wadda shekarunta sun wuce, ta iya haifi 'ya'ya domin ta
† **11:18** Far 21.12

29 Ta wurin bangaskiya ne mutane suka bi ta cikin Jan Teku, sai ka ce a kan
busasshiyar ƙasa; amma da Masarawa suka yi ƙoƙari su yi haka, sai aka nutsar
da su.
30 Ta wurin bangaskiya ne katangar Yeriko ta rushe, bayan mutane suka yi ta
kewaye ta har kwana bakwai.
31 Ta wurin bangaskiya ne ba a kashe Rahab karuwan nan, ta tare da marasa
biyayya ba don ta marabci ’yan leƙan asiri.
32 Me kuma zan faɗa? Ba ni da lokacin da zan ba da labari a kan Gideyon,
Barak, Samson, Yefta, Dawuda, Sama’ila, da kuma annabawa, 33 waɗanda ta wurin
bangaskiya ne suka ci nasara a kan mulkoki, suka aikata adalci, suka kuma sami abin
da aka yi alkawari; waɗanda suka rurrufe bakunan zakoki, 34 suka kashe harshen
wuta, suka kuma tsere wa kaifin takobi; waɗanda aka mai da rashin ƙarfinsu ya zama
ƙarfi; waɗanda suka yi jaruntaka wajen yaƙi suka kuma fatattaki mayaƙan waɗansu
ƙasashe. 35 Mata suka karɓi ƙaunatattunsu da aka sāke tasar daga matattu. Aka
azabtar da yawancin mutanen nan, amma suka ƙi a sake su, domin sun tabbata za
su sami lada mafi kyau sa’ad da aka tā da matattu. 36 Waɗansu suka sha ba’a da
bulala, har da dauri da sarƙa, da kuma jefa su cikin kurkuku. 37 Aka jajjefe su da
duwatsu; aka raba su biyu da zarto; aka kashe su da takobi. Suka yi ta yawo saye da
fatun tumaki da na awaki, suka yi zaman rashi, suka sha tsanani da kuma wulaƙanci
38 duniya ba tă ma cancanci su zauna a cikinta ba. Suka yi ta yawo a cikin hamada
da a kan duwatsu, da cikin kogwanni da kuma cikin ramummuka.
39 Waɗannan duka an yabe su saboda bangaskiyarsu, duk da haka babu waninsu
da ya sami abin da aka yi alkawari. 40 Allah ya shirya mana wani abu mafi kyau.
Kuma bai so su kai ga maƙasudin bangaskiyarsu ba sai tare da mu.

# 12

1 Saboda haka, da yake muna kewaye da irin wannan taron shaidu mai girma, sai
mu yar da duk abin da yake hana mu da kuma zunubin da yake saurin daure mu,
mu kuma yi tseren da aka sa a gabanmu da nacewa. 2 Bari mu kafa idanunmu a kan
Yesu, tushe da kuma kammalar bangaskiyarmu, wanda ya jure kunyar gicciye da aka
yi masa, domin ya san cewa daga baya zai yi farin ciki ya yi haka. Yanzu kuma yana
zaune a hannun dama na kursiyin Allah. 3 Ku lura da wannan wanda ya jure da irin
hamayyan nan daga masu zunubi, don kada ku gaji, har ku fid da zuciya.

### *Allah yakan hori ’ya’yansa*

4 Cikin famanku da zunubi, ba ku yi tsayayya har ga zub da jininku ba tukuna.
5 Kun kuma manta da kalmar ƙarfafawan nan da tana ce da ku ’ya’ya,
“Ɗana kada ka rena horon Ubangiji,
kada kuma ka fid da zuciya sa’ad da ya kwaɓe ka,
6 domin Ubangiji yakan hori waɗanda yake ƙauna,
yakan kuma hori duk wanda yakan karɓa a matsayin ɗa.”*
7 Ku jimre shan wahala a matsayin horo; Allah yana yi da ku kamar ’ya’ya. Gama
wane ɗa ne mahaifinsa ba ya horonsa? 8 In ba a hore ku ba (kowa kuwa yakan
sami horo), to, ku shegu ne ba ’ya’yan gida ba. 9 Ban da haka ma, dukanmu mun
kasance da ubannin jiki waɗanda suka hore mu muka kuma yi musu ladabi. Ashe,
bai kamata mu yi wa Uban ruhohinmu biyayya mu kuwa rayu ba! 10 Ubanninmu
sun hore mu na ɗan lokaci yadda suka ga ya fi kyau; amma Allah yakan hore mu
don amfaninmu, domin mu sami rabo cikin tsarkinsa. 11 Babu horon da yake da daɗi
a lokacin da ake yinsa, sai dai zafi. Amma daga baya waɗanda suka horu ta haka
sukan sami kwanciyar rai wadda aikin adalci yake bayarwa.

* **12:6** K Mag 3.11,12

12 Saboda haka, sai ku ƙarfafa raunanan hannuwanku da gwiwoyinku marasa
ƙarfi! 13 "Ku shirya hanyoyi marasa gargaɗa saboda ƙafafunku,"† don kada guragu
su daɗa gurguntawa, sai dai su warke.

### *Gargaɗi game da ƙin Allah*

14 Ku yi iyakacin ƙoƙari ku yi zaman lafiya da kowa, ku kuma zama masu tsarki;
gama in ban da tsarki ba babu wanda zai ga Ubangiji. 15 Ku lura fa kada wani yă
kāsa samun alherin Allah, kada kuma wani tushen ɗacin rai yă tsira har yă kawo
rikici, yă kuma ƙazantar da mutane da yawa. 16 Ku lura kada wani yă zama mai
fasikanci, ko marar tsoron Allah kamar Isuwa, wanda saboda ƙwaryar abinci ɗaya
tak ya sayar da gādonsa na ɗan fari. 17 Daga baya, kamar yadda kuka sani, sa'ad da
ya nemi yă gāji wannan albarka, aka ƙi shi. Bai sami zarafin tuba ba, ko da yake ya
nemi albarkan nan da hawaye.

### *Dutsen tsoro da kuma dutsen farin ciki*

18 Ba ku zo ga Dutsen Sinai‡ wanda ana iya taɓawa ba, ko ga wuta mai ci sosai,
ko ga duhu baƙi ƙirin, ko 19 ko busar ƙaho, ko ga irin wata murya mai magana da
kalmomin da masu jinta suka yi roƙo kada su ƙara ji, 20 domin ba su iya jimrewa
da abin da aka umarta cewa, "Ko da ma dabba ce ta taɓa dutsen, dole a jajjefe ta da
duwatsu."§ 21 Ganin wannan abu da matuƙar bantsoro yake, har Musa ya ce, "Ina
rawar jiki don tsoro."*
22 Sai dai kun zo ne ga Dutsen Sihiyona, ga Urushalima ta sama, birnin Allah mai
rai. Kun zo ga dubu dubban mala'ikun da suke cikin taron farin ciki, 23 kun zo ga
ikkilisiyar ɗan fari, waɗanda sunayensu suna a rubuce a sama. Kun zo ga Allah,
alƙalin dukan mutane, kun kuma zo ga ruhohin mutane masu adalci da aka mai da
su cikakku. 24 Kun zo ga Yesu, mai yin sulhu na sabon alkawari, da kuma ga jinin da
aka yayyafa wanda yake magana mafi kyau fiye da jinin Habila.
25 Ku lura fa kada ku ƙi wanda yake magana. Gama in su ba su tsira sa'ad da suka
ƙi wanda ya gargaɗe su a wannan duniya ba, to, ƙaƙa mu za mu tsira, in mun ƙi jin
wannan da yake yi mana gargaɗi daga Sama? 26 A lokacin nan muryarsa ta jijjiga
duniya, amma yanzu ya yi alkawari cewa, "Har wa yau sau ɗaya tak zan ƙara jijjiga
ba duniya kaɗai ba, amma har ma da sammai."† 27 Wannan magana "sau ɗayan
nan" sun nuna, kawar da abin da za a iya jijjigawa, wato, ƙirƙiro abubuwa, saboda
abubuwan da ba a iya jijjigawa, su kasance.
28 Saboda haka, da yake muna karɓar mulkin da ba ya jijjiguwa, sai mu yi godiya,
ta haka kuwa mu yi wa Allah sujada yadda ya kamata, tare da bangirma da kuma
tsoro, 29 gama "Allahnmu wuta ne mai cinyewa."‡

# 13

### *Gargaɗin ƙarshe*

1 Ku ci gaba da ƙaunar juna kamar 'yan'uwa. 2 Kada ku manta da yin alheri ga
baƙi, gama ta yin haka ne waɗansu suka yi wa mala'iku hidima, ba da saninsu ba.
3 Ku riƙa tunawa da waɗanda suke a kurkuku kamar tare kuke a kurkuku, da kuma
waɗanda ake gwada musu azaba, kamar ku ake yi wa.
4 Aure yă zama abin girmamawa ga kowa, a kuma kiyaye gadon aure da tsabta,
gama Allah zai hukunta masu zina da kuma dukan masu fasikanci. 5 Ku kiyaye
kanku daga yawan son kuɗi, ku kuma gamsu da abin da kuke da shi, gama Allah ya
ce,

---

† **12:13** K Mag 4.26 ‡ **12:18** Dutsen Sinai. Wato, inda Allah ya ba wa annabi Musa dokoki domin Isra'ilawa
§ **12:20** Fit 19.12,13 * **12:21** Dubi M Sh 9.19. † **12:26** Hag 2.6 ‡ **12:29** M Sh 4.24

"Ba zan taɓa bar ka ba;
ba zan taɓa yashe ka ba."*
6 Saboda haka muna iya fitowa gabagadi, mu ce,
"Ubangiji ne mai taimakona; ba zan ji tsoro ba.
Me mutum zai iya yi mini?"†
7 Ku tuna da shugabanninku, waɗanda suka faɗa muku maganar Allah. Ku dubi
irin rayuwar da suka yi ku kuma yi koyi da bangaskiyarsu. 8 Yesu Kiristi ba ya
sākewa, shi ne a jiya, shi ne a yau, shi ne kuma har abada.
9 Kada a ɗauke muku hankali da sababbin koyarwa dabam-dabam. Yana da kyau
zukatanmu su ƙarfafa ta wurin alheri, ba ta wurin abinci waɗanda ba su da amfani
ga waɗanda suke cinsu. 10 Muna da bagade inda firistocin da suka yi hidima a
tabanakul ba su da izini su ci.
11 Babban firist yakan ɗauki jinin dabbobi yă shiga cikin Wuri Mafi Tsarki a
matsayin hadaya ta zunubi, amma jikunan dabbobin akan ƙone su a bayan sansani.
12 Haka ma Yesu ya sha wahala a bayan gari don yă tsarkake mutane ta wurin jininsa.
13 Saboda haka, sai mu fita mu je wajensa a bayan sansani, muna ɗaukar kunyar da
ya sha. 14 Gama a nan ba mu da dawwammamen birni, sai dai muna zuba ido a kan
birnin nan mai zuwa.
15 Saboda haka, ta wurin Yesu, bari mu ci gaba da miƙa hadaya ta yabo ga Allah,
yabon leɓuna da yake shaidar sunansa. 16 Kada kuma ku manta yin aikin nagari da
kuma taimakon waɗansu, gama da irin waɗannan hadayu ne Allah yake jin daɗi.
17 Ku yi wa shugabanninku biyayya ku kuma miƙa kanku ga ikonsu. Suna lura da
ku kuma za su ba da lissafi a gaban Allah. Saboda haka kada ku sa su yi fushi saboda
aikinsu, ku sa su yi farin ciki. In ba haka ba za su iya taimakonku ba ko kaɗan.
18 Ku yi mana addu'a. Mun tabbata cewa muna da lamiri mai kyau, kuma muna
da marmari mu yi rayuwa ta bangirma a ta kowace hanya. 19 Ni musamman, ina
roƙonku ku yi addu'a, don a komo da ni a gare ku ba da daɗewa ba.

### *Albarka da kuma gaisuwa ta ƙarshe*

20 Bari Allah na salama, wanda ta wurin jinin madawwamin alkawari ya tā da
Ubangijinmu Yesu daga matattu, wannan Makiyayin tumaki mai girma, 21 yă kintsa
ku da kowane abu mai kyau domin aikata nufinsa, bari kuma yă aikata abin da zai
gamshe shi cikinmu, ta wurin Yesu Kiristi, a gare shi ɗaukaka ta tabbata har abada.
Amin.

22 'Yan'uwa, ina roƙonku ku yi haƙuri da wannan gargaɗi, don ba wata doguwar wasiƙa ce na rubuta muku ba.

23 Ina so ku san cewa an saki ɗan'uwanmu Timoti. In ya iso da wuri, zan zo tare da shi in gan ku.

24 Ku gai da dukan shugabanninku da kuma dukan mutanen Allah.
Waɗanda suke Italiya suna gaishe ku.

25 Alheri yă kasance da ku duka.

---

* **13:5** M Sh 31.6 † **13:6** Zab 118.6,7

# Yaƙub

1 Yaƙub, bawan Allah da kuma na Ubangiji Yesu Kiristi,

Zuwa ga kabilan nan goma sha biyu, da suke warwartse a cikin al'ummai.

Gaisuwa mai yawa.

### *Gwaje-gwaje da jarrabobi*

2 Ku ɗauki wannan da farin ciki mai tsabta, 'yan'uwana, duk sa'ad da gwaje-gwaje
na kowane iri suka zo muku, 3 domin kun san cewa gwajin bangaskiyarku yakan
haifi daurewa. 4 Dole daurewa ta kammala aikinta don ku zama balagaggu da kuma
cikakku, ba ku kuma rasa kome ba. 5 In waninku ya rasa hikima, ya kamata yǎ roƙi
Allah, mai bayarwa hannu sake ga kowa ba tare da gori ba, za a kuwa ba shi. 6 Amma
sa'ad da ya roƙa, dole yǎ gaskata, ba tare da shakka ba, domin shi mai shakka, yana
kama da raƙumar ruwan tekun da iska take kori tana kuma ɓuɓɓugowa. 7 Kada irin
wannan mutum yǎ yi tsammani zai sami wani abu daga Ubangiji; 8 shi mai zuciya
biyu ne, marar tsai da zuciyarsa wuri ɗaya a cikin duk abin da yake yi.
9 Bari ɗan'uwan da yake cikin halin ƙasƙanci yǎ yi taƙama a matsayinsa na
ɗaukaka. 10 Amma wanda yake mai arziki, ya kamata yǎ yi taƙama a matsayinsa
na ƙasƙanci, gama ba zai daɗe ba kamar furen jeji. 11 Gama in rana ta fito ta yi zafi
mai tsanani sai ta sa tsiro yǎ yanƙwane tsiro; furensa yǎ kakkaɓe, kyansa kuma yǎ
lalace. Haka ma mai arziki zai shuɗe yayinda yake cikin harkarsa.
12 Mai albarka ne mutumin da yake daurewa cikin gwaji, gama bayan ya yi nasara
da gwajin, zai sami rawanin rai wanda Allah ya yi alkawari ga waɗanda suke
ƙaunarsa.
13 Sa'ad da aka jarrabci mutum, kada yǎ ce, "Allah ne yake jarrabtarsa." Gama ba
ya yiwuwa a jarrabci Allah da mugunta, shi kuma ba ya jarrabtar kowa; 14 amma
akan jarrabce kowane mutum sa'ad da muguwar sha'awarsa ta janye shi ta kuma
rinjaye shi. 15 Sa'an nan, bayan da sha'awar ta yi ciki, takan haifi zunubi; zunubi
kuwa, sa'ad da ya balaga yakan haifi mutuwa.
16 Kada a ruɗe ku, 'yan'uwana ƙaunatattu. 17 Kowane abu mai kyau da kuma
kowace cikakkiyar kyauta daga sama suke, sun sauko ne daga wurin Uban haskoki,
wanda ba sauyawa ko wata alamar sākewa a gare shi faufau. 18 Ya zaɓa yǎ haife mu
ta wurin kalmar gaskiya, domin mu zama 'ya'yan fari na dukan abin da ya halitta.

### *Saurarawa da kuma aikatawa*

19 'Yan'uwana ƙaunatattu, ku lura da wannan. Ya kamata kowa yǎ kasance mai
saurin saurara, ba mai saurin magana ba, ba kuma mai saurin fushi ba, 20 gama
fushin mutum ba ya kawo rayuwar adalcin da Allah yake so. 21 Saboda haka, ku
rabu da ƙazamin hali da kuma kowace irin mugunta ku kuma yi na'am da maganar
da aka shuka a cikinku da tawali'u, wadda za tǎ iya cetonku.
22 Kada ku zama masu ji kawai, ku ruɗi kanku. A maimakon haka ku zama masu
yin abin da ta ce. 23 Duk wanda yake ji magana ne kawai, bai kuwa aikata abin da ta
ce ba, yana kama da mutumin da ya kalli fuskarsa a madubi 24 bayan ya kalli kansa,
sa'ad da ya tashi daga wurin, nan da nan sai yǎ manta da kamanninsa. 25 Amma duk
mai duba cikakkiyar ƙa'idan nan ta 'yanci, ya kuma nace a kanta, ya zama ba mai ji
ne kawai yǎ mance ba, sai dai mai yi ne yǎ zartar, to wannan shi za a yi wa albarka
a cikin abin da yake yi.

26 In wani ya ɗauki kansa mai addini ne duk da haka bai ƙame harshensa ba, ruɗin
kansa yake yi addininsa kuwa banza ne. 27 Addinin da Allah Ubanmu ya yarda da
shi a matsayin mai tsabta da kuma marar aibi shi ne, a kula da marayu da gwauraye
cikin damuwoyinsu, a kuma kiyaye kai daga lalacin da duniya take sa wa.

# 2

*Kada a nuna bambanci*

1 ʼYanʼuwana, a matsayinmu cikin Ubangiji Yesu Kiristi maɗaukaki, kada ku nuna
bambanci. 2 A ce wani ya shigo cikin taronku saye da zoben zinariya da riguna masu
tsada, wani matalauci kuma saye da tsummoki shi ma ya shigo, 3 in kuka mai da
hankali na musamman ga mutumin da yake da riguna masu tsadan nan kuka kuma
ce, “Ga wurin zama mai kyau dominka,” amma kuka ce wa matalaucin nan, “Kai
tsaya daga can,” ko kuwa, “Ka zauna a ƙasa kusa da ƙafafuna,” 4 ashe, ba ku nuna
bambanci a tsakaninku ke nan ba, kuka kuma zama alƙalai masu mugayen tunani?
5 Ku saurara, ʼyanʼuwana ƙaunatattu. Ashe, Allah bai zaɓi waɗanda suke
matalauta a idon duniya don su zama masu wadata cikin bangaskiya, su kuma gāji
mulkin da ya yi wa masu ƙaunarsa alkawari ba? 6 Ga shi kun wulaƙanta matalauta.
Ashe, ba masu arziki ne suke cutarku ba? Ba su ba ne suke jan ku zuwa kotu? 7 Ba
su ba ne suke ɓata sunan nan mai martaba wanda aka san ku da shi ba?
8 In fa kun kiyaye dokan nan ta mulki wadda take cikin Nassi mai cewa, “Kaunaci
maƙwabcinka kamar kanka,”* kun yi daidai. 9 Amma in kuka nuna bambanci, kun yi
zunubi ke nan shariʼa kuma ta same ku da laifi a matsayin masu karya doka. 10 Gama
duk wanda ya kiyaye dukan doka amma ya yi tuntuɓe a kan abu ɗaya kaɗai, ya zama
mai laifin karya dukansu ke nan. 11 Gama shi da ya ce, “Kada ka yi zina,”† shi ne
kuma ya ce, “Kada ka yi kisankai.”‡ In kuwa ba ka zina amma kana kisankai, ka
zama mai karya doka ke nan.
12 Ku yi magana ku kuma yi aiki kamar waɗanda za a yi musu shariʼa bisa ga doka
mai ba da ʼyanci, 13 gama za a yi wa duk wanda bai nuna jinƙai ba hukunci babu
jinƙai. Jinƙai yakan yi nasara a kan hukunci!

*Bangaskiya da ayyuka*

14 Wanda amfani ne, ʼyanʼuwana, a ce wani yǎ ce yana da bangaskiya, amma ba shi
da ayyuka? Anya, wannan bangaskiya za tǎ iya cetonsa kuwa? 15 A ce wani ɗanʼuwa
ko ʼyarʼuwa ba shi da riguna ko abincin yini, 16 sai waninku yǎ ce masa, “Sauka lafiya,
Allah ya ba da ci da sha da kuma sutura,” amma bai yi wani abu game da bukatunsa
na jiki ba, ina amfani? 17 Haka ma bangaskiya ita kaɗai, in ba tare da ayyuka ba,
matacciya ce.
18 Amma wani zai ce, “Kai kana da bangaskiya; ni kuma ina da ayyuka.”
Ka nuna mini bangaskiyarka ba tare da ayyuka ba, ni kuma zan nuna maka
bangaskiyata ta wurin abin da nake yi. 19 Ka gaskata cewa Allah ɗaya ne. To, da
kyau! Ai, ko aljanu ma sun gaskata wannan, har da rawan jiki.
20 Kai wawa, kana son tabbaci cewa bangaskiya marar ayyuka banza ce? 21 Ashe,
ba a mai da kakanmu Ibrahim mai adalci saboda abin da ya yi ba ne saʼad da ya
miƙa ɗansa Ishaku a bisa bagade? 22 Ai, ka gani cewa bangaskiyarsa da ayyukansa
sun yi aiki tare, bangaskiyarsa kuma ta zama cikakkiya ta wurin abin da ya yi. 23 Aka
kuma cika nassin nan da ya ce, “Ibrahim ya gaskata Allah, aka kuma lissafta wannan
adalci ne gare shi,”§ aka kuma ce da shi abokin Allah. 24 Kun ga cewa ashe mutum
zai sami kuɓuta ta wurin abin da ya yi ne ba ta wurin bangaskiya kaɗai ba.

---

* **2:8** Fir 19.18 † **2:11** Fit 20.14; M Sh 5.18 ‡ **2:11** Fit 20.13; M Sh 5.17 § **2:23** Far 15.6

25 Ta haka kuma ashe, Rahab karuwan nan ba a ɗauke ta mai adalci ce saboda
abin da ta yi ba ne sa'ad da ta ba wa 'yan leƙen asirin nan masauƙi ta kuma sallame
su suka tafi ta wata hanya dabam? 26 Kamar yadda jikin da babu ruhu matacce ne,
haka ma bangaskiyar da babu ayyuka matacciya ce.

# 3

*Kamewa harshe*

1 Kada yawancinku su so ɗaukan kansu a matsayin malamai, 'yan'uwana, domin
kun san cewa mu da muke koyarwa za a yi mana shari'a mafi tsanani. 2 Dukanmu
mukan yi tuntuɓe a hanyoyi dabam-dabam. In wani bai taɓa yin kuskure a cikin
maganarsa ba, shi cikakke ne, yana kuma iya ƙame dukan jikinsa.
3 Sa'ad da muka sa linzamai a bakunan dawakai don mu sa su yi mana biyayya,
mukan iya bin da dabbar gaba ɗaya. 4 Ko kuwa misali, mu dubi jiragen ruwa, mana.
Ko da yake suna da girma ƙwarai kuma iska mai ƙarfi ce take tura su, ana tuƙa su
da ɗan ƙaramin sandan ƙarfe ne zuwa duk inda mai tuƙin jirgin yake so. 5 Haka ma
harshe yake, ga shi ɗan ƙanƙanin gaɓar jiki ne, amma sai manyan fariya. Ku dubi
yadda ɗan ƙaramin ƙyastu yake ƙuna wa babban jeji wuta mana. 6 Harshe ma wuta
ne! A cikin duk gaɓoɓinmu, harshe shi ne tushen kowace irin mugunta, mai ɓata
mutum gaba ɗaya, mai zuga zuciyar mutum ta tafasa, shi kuwa jahannama ce take
zuga shi.
7 Kowace irin dabba, tsuntsu, masu ja da ciki da kuma halittun da suke cikin teku
an sarrafa su kuma mutum ne ya sarrafa, 8 amma ba mutumin da zai iya ya sarrafa
harshe. Mugu ne marar hutu, cike da dafi mai kisa.
9 Da harshe mukan yabi Ubangijinmu da kuma Ubanmu, da shi kuma muke la'antar
mutane, waɗanda aka halitta a kamannin Allah. 10 Daga wannan baki guda yabo da
la'ana suke fitowa. 'Yan'uwana, wannan bai kamata yă zama haka ba. 11 Ruwa mai
kyau da kuma ruwan gishiri zai iya fito daga maɓulɓula ɗaya? 12 'Yan'uwana, itacen
ɓaure yana iya haifar 'ya'yan zaitun, ko kuma itacen inabi yă haifi 'ya'yan ɓaure?
Haka ma, maɓulɓular ruwan gishiri ba zai iya ba da ruwa mai kyau ba.

*Hikima iri biyu*

13 Wane ne mai hikima da fahimta a cikinku? Bari yă nuna ta ta wurin rayuwarsa
mai kyau, ta wurin ayyukan da aka yi cikin tawali'un da suke fitowa daga hikima.
14 Amma in kuna cike da mugun kishi da kuma sonkai a cikin zukatanku, kada ku
yi taƙama game da wannan, ko ku danne gaskiya. 15 Irin wannan "hikima" ba daga
sama ta sauko ba, ta duniya ce, ta rashin ruhaniya, ta Iblis kuma. 16 Gama inda akwai
kishi da sonkai, a can za a tarar da hargitsi da kowane irin mugun aiki.
17 Amma hikimar da ta zo daga sama da fari tana da tsabta gaba ɗaya; sa'an nan
mai ƙaunar salama ce, mai sanin ya kamata, mai biyayya, cike da jinƙai da aiki mai
kyau, marar nuna bambanci, sahihiya kuma. 18 Masu salama da suke shuki cikin
salama sukan girbe adalci.

# 4

*Miƙa kanku ga Allah*

1 Me yake jawo faɗace-faɗace da gardandami a tsakaninku? Ashe, ba sha'awace-
sha'awacenku da suke yaƙi a zukatanku ba ne? 2 Kukan nemi abu ku rasa, sai ku
yi kisa da ƙyashi. In kuka rasa abin da kuke nema sai ku shiga yin gardama da
faɗa. Kukan rasa ne, domin ba ku roƙi Allah ba. 3 Sa'ad da kuka roƙa, ba kwa samu,
don kun roƙa da mugun nufi, don ku kashe abin da kuka samu a kan sha'awace-
sha'awacenku.

4 Ku mazinata, ba ku san cewa abokantaka da duniya gāba ce da Allah ba? Duk
wanda ya zaɓa yă zama abokin duniya ya zama abokin gāban Allah ke nan. 5 Ko
kuna tsammani a banza ne Nassi ya ce ruhun da ya sa yă zauna a cikinmu yana kishi
sosai? 6 Amma yakan ba mu alheri a yalwace. Shi ya sa Nassi ya ce,
"Allah yana gāba da masu girman kai
amma yakan ba da alheri ga masu tawali'u."*
7 Saboda haka, ku miƙa kanku ga Allah. Ku yi tsayayya da Iblis, zai kuwa guje ku.
8 Ku matso kusa da Allah shi kuwa zai matso kusa da ku. Ku wanke hannuwanku, ku
masu zunubi, ku kuma tsarkake zukatanku, ku masu zuciya biyu. 9 Ku yi baƙin ciki,
ku yi makoki ku kuma yi kuka. Ku mai da dariyarku ta zama makoki, farin cikinku
kuma yă zama ɓacin zuciya. 10 Ku ƙasƙantar da kanku a gaban Ubangiji, zai kuwa
ɗaukaka ku.
11 'Yan'uwa, kada ku ɓata wa juna suna. Duk wanda ya zargi ɗan'uwansa ko ya
ɗora masa laifi, yana gāba da doka ne yana kuma yin mata shari'a ke nan. In kuwa
ka ɗora wa shari'a laifi, kai ba mai binta ba ne, mai ɗora mata laifi ne. 12 Akwai
Mai ba da doka da kuma Alƙali guda ɗaya tak, shi ne yake da ikon ceto da kuma
hallakarwa. Amma kai, wane ne da za ka hukunta maƙwabcinka?

### *Yin fahariya game da gobe*

13 Yanzu fa sai ku saurara, ku da kuke cewa, "Yau ko gobe za mu je wannan ko
wancan birni, mu yi shekara a can, mu yi kasuwanci, mu ci riba." 14 Alhali kuwa ba
ku ma san abin da zai faru gobe ba. Wane iri ne ranku? Ku kamar hazo ne da yake
bayyana na ɗan lokaci sa'an nan yă ɓace. 15 A maimakon haka, ya kamata ku ce,
"In Ubangiji ya yarda, muna kuma a raye, za mu yi wannan ko wancan." 16 Ga shi,
kuna fariya da taƙama. Duk irin wannan taƙama mugun abu ne. 17 Saboda haka,
duk wanda ya san abu mai kyan da ya kamata yă yi, bai kuwa yi ba, ya yi zunubi ke
nan.

## 5

### *Gargaɗi ga masu arziki masu danniya*

1 Yanzu fa sai ku saurara, ku masu arziki, ku yi kuka da ihu, saboda azabar da take
zuwa a kanku. 2 Arzikinku ya ruɓa, asu kuma sun cinye tufafinku. 3 Zinariyarku
da azurfarku sun yi tsatsa. Tsatsarsu kuwa za tă zama shaida a kanku, ta kuma ci
namar jikinku kamar wuta. Kun ɓoye dukiya a kwanakin ƙarshe. 4 Ga shi! Zaluncin
da kuka yi na hakkin ma'aikatan gonakinku yana ta ƙara. Kukan masu girbi ya kai
kunnuwan Ubangiji Maɗaukaki. 5 Kun yi rayuwar jin daɗi a duniya kuna ci kuna
sha na ganin dama. Kun ciyar da kanku kun yi ƙiba don ranar yanka. 6 Kun hukunta
kun kuma kashe mutane marasa laifi, waɗanda ba su yi gāba da ku ba.

### *Haƙuri cikin wahala*

7 Saboda haka 'yan'uwa, sai ku yi haƙuri har dawowar Ubangiji. Ku dubi yadda
manomi yakan jira gona ta ba da amfaninta mai kyau, da kuma yadda yake haƙurin
jiran ruwan sama na damina da na kaka. 8 Haka ku ma, ku yi haƙuri, ku tsaya da
ƙarfi, gama dawowar Ubangiji ya yi kusa. 9 'Yan'uwa, kada ku yi gunaguni da juna,
don kada a hukunta ku. Alƙalin yana tsaye a bakin ƙofa!
10 'Yan'uwa, ku ɗauki annabawa da suka yi magana a cikin sunan Ubangiji, a
matsayin gurbi na haƙuri a cikin shan wahala. 11 Kamar yadda kuka sani, mukan ce
da waɗanda suka jure, masu albarka ne. Kun ji daurewar Ayuba, kuka kuma ga abin
da Ubangiji ya yi a ƙarshe. Ubangiji yana cike da tausayi da jinƙai.

* **4:6** K Mag 3.34

12 ’Yan’uwana, fiye da kome, kada ku yi rantsuwa ko da sama, ko da ƙasa ko da
wani abu dabam. Bari “I” naku yă zama “I”. “A’a” naku kuma yă zama “A’a”, don
kada a hukunta ku.

*Addu’ar bangaskiya*

13 Akwai waninku da yake shan wahala? Ya kamata yă yi addu’a. Akwai wani
mai murna? Sai yă rera waƙoƙin yabo. 14 Akwai waninku da yake ciwo? Ya kamata
yă kira dattawan ikkilisiya su yi masa addu’a, su kuma shafa masa mai cikin sunan
Ubangiji. 15 Addu’ar da aka yi cikin bangaskiya, za tă warkar da marar lafiya, Ubangiji
zai tashe shi. In ya yi zunubi kuwa za a gafarta masa. 16 Saboda haka, ku furta wa
juna zunubanku, ku yi addu’a saboda juna, domin ku sami warkarwa. Addu’ar mai
adalci tana da iko da kuma amfani.
17 Iliya mutum ne kamar mu. Ya yi addu’a da gaske don kada a yi ruwan sama, ba
a kuma yi ruwan sama a ƙasar ba har shekaru uku da rabi. 18 Ya sāke yin addu’a,
sai sammai suka ba da ruwan sama, ƙasa kuma ta ba da amfaninta.
19 ’Yan’uwana, in waninku ya kauce daga gaskiya, wani kuma ya komo da shi, 20 sai
yă tuna da wannan. Duk wanda ya komo da mai zunubi daga kaucewarsa, zai cece
shi daga mutuwa, yă kuma rufe zunubai masu ɗumbun yawa.

# 1 Bitrus

1 Bitrus, manzon Yesu Kiristi,

Zuwa ga zaɓaɓɓu na Allah, baƙi a duniya, da suke a warwatse ko'ina a Fontus,
Galatiya, Kaffadokiya, Asiya da kuma Bitiniya, 2 waɗanda aka zaɓa bisa ga rigyasanin
Allah Uba, ta wurin aikin tsarkakewar Ruhu, don biyayya ga Yesu Kiristi, su kuma
sami yayyafan jininsa.

Alheri da salama su zama naku a yalwace.

### *Yabo ga Allah domin bege mai rai*

3 Yabo ya tabbata ga Allah Uban Ubangijinmu Yesu Kiristi! Cikin jinƙansa mai
girma ya ba mu sabuwar haihuwa cikin bege mai rai ta wurin tashin Yesu Kiristi
daga matattu, 4 da kuma cikin gādon da ba zai taɓa lalacewa, ɓacewa ko koɗewa ba,
ajiyayye a sama dominku, 5 ku waɗanda ta wurin bangaskiya ake kiyayewa ta wurin
ikon Allah har yă zuwa ceton da yake a shirye da za a bayyana a ƙarshen lokaci. 6 A
kan wannan kuke cike da farin ciki ƙwarai, ko da yake yanzu na ɗan lokaci kuna
fuskantar baƙin ciki daga gwaje-gwaje iri-iri. 7 Wannan kuwa domin a tabbatar da
sahihancin bangaskiyarku ne, wadda ta fi zinariya daraja nesa, ita zinariya kuwa, ko
da yake mai ƙarewa ce, akan gwada ta da wuta, domin bangaskiyan nan taku ta jawo
muku yabo da girma da ɗaukaka a bayyanar Yesu Kiristi. 8 Ko da yake ba ku taɓa
ganinsa ba, kuna ƙaunarsa; kuma ko da yake ba kwa ganinsa yanzu, kun gaskata
shi, kun kuma cika da farin ciki ƙwarai, wanda ya fi gaban faɗi, 9 gama kuna samun
sakamakon bangaskiyarku, ceton rayukanku ke nan.
10 Game da ceton nan, annabawa, waɗanda suka yi maganar alherin da za tă zo
gare ku, sun yi bincike mai zurfi, a natse, 11 suna ƙoƙari su san lokaci da kuma
yanayin da Ruhun Kiristi da yake cikinsu yana nunawa sa'ad da ya yi faɗi a kan
wahalolin Kiristi da kuma ɗaukaka da za tă bi. 12 Aka bayyana musu cewa ba kansu
ne suke bauta wa ba sai ku, sa'ad da suka yi maganar abubuwan da aka faɗa muku
ta wurin waɗanda suka yi muku wa'azin bishara, ta wurin Ruhu Mai Tsarki wanda
aka aika daga sama. Ko mala'iku ma suna marmari su ga waɗannan abubuwa.

### *Ku zama masu tsarki*

13 Saboda haka, ku shirya kanku don aiki; ku zama masu kamunkai; ku kafa
begenku duka a kan alherin da za a ba ku sa'ad da aka bayyana Yesu Kiristi. 14 Kamar
'ya'ya masu biyayya, kada ku bi mugayen sha'awace-sha'awacen da dā kuke da su
sa'ad da kuke rayuwa a cikin jahilci. 15 Amma kamar yadda wanda ya kira ku yake
mai tsarki, haka ku ma sai ku kasance masu tsarki cikin dukan abubuwan da kuke
yi; 16 gama a rubuce yake cewa, "Ku zama masu tsarki, domin ni mai tsarki ne."*
17 Tun da yake kuna kira ga Uba wanda yake yin wa kowane mutum shari'a bisa
ga ayyukansa ba bambanci, sai ku yi rayuwarku a nan kamar baƙi cikin tsoro mai
bangirma. 18 Gama kun san cewa ba da abubuwa masu lalacewa kamar azurfa
ko zinariya ce aka fanshe ku daga rayuwar banza da kuka karɓa daga kakanni-
kakanninku ba, 19 sai dai an fanshe ku da jini mai daraja na Kiristi, ɗan rago marar
aibi ko lahani. 20 An zaɓe shi kafin halittar duniya, amma an bayyana shi a zamanin
ƙarshe saboda ku. 21 Ta gare shi ne kuka gaskata da Allah, wanda ya tā da shi daga

* **1:16** Fir 11.44,45; Fir 19.2; Fir 20.7

matattu, aka kuma ɗaukaka shi, ta haka bari bangaskiyarku da begenku su kasance
ga Allah.
22 Yanzu da kuka tsarkake kanku ta wurin yin biyayya ga gaskiyan nan, don ku
kasance da ƙauna mai gaskiya wa 'yan'uwanku, sai ku ƙaunaci juna ƙwarai, daga
zuciya. 23 Gama an sāke haihuwarku, ba da iri da yake lalacewa ba, sai dai marar
lalacewa, ta wurin rayayyiya da kuma madawwamiyar maganar Allah. 24 Gama,
"Dukan mutane kamar ciyawa suke,
darajarsu kuma kamar furannin jeji ne;
ciyawa takan yanƙwane furannin kuma su kakkaɓe,
25 amma maganar Ubangiji tana nan har abada."†
Wannan kuwa ita ce kalmar da aka yi muku wa'azi.

# 2

1 Saboda haka, ku rabu da kowace ƙeta da dukan ruɗu, munafunci, kishi, da kuma
kowace irin ɓata suna. 2 Kamar sababbin jarirai, ku yi marmarin madara zalla ta
ruhaniya, domin ta wurinta za ku yi girma cikin cetonku, 3 yanzu da kuka ɗanɗana
alherin Ubangiji.

### *Dutse mai rai da kuma zaɓaɓɓun mutane*

4 Da kuka zo gare shi, rayayyen Dutse, da mutane suka ƙi amma Allah ya zaɓa,
kuma mai daraja a gare shi 5 ku ma, a matsayinku na duwatsu masu rai, ana gina
ku ga zama gidan ruhaniya don ku zama tsattsarkar ƙungiyar firistoci, kuna miƙa
hadayun ruhaniya, abin karɓa ga Allah ta wurin Yesu Kiristi. 6 Gama a cikin Nassi
an ce,
"Ga shi, na kafa dutse a Sihiyona,
zaɓaɓɓen dutse na kusurwar gini mai daraja,
wanda kuma ya dogara gare shi
ba zai taɓa kunyata ba."*
7 A gare ku da kuka gaskata, wannan dutse mai daraja ne. Amma ga waɗanda ba su
gaskata ba,
"Dutsen da magina suka ƙi
ya zama dutsen kusurwar gini,†
8 kuma,
"Dutse ne da yake sa mutane tuntuɓe
kuma fā ne da yake sa su fāɗi."‡
Sun yi tuntuɓe domin sun ƙi su yi biyayya da saƙon, wanda kuma yake abin da aka
ƙaddara musu.
9 Amma ku zaɓaɓɓu ne, ƙungiyar firistocin babban Sarki, al'umma mai tsarki,
jama'a mallakar Allah, domin ku shaida yabon shi wanda ya kira ku daga cikin duhu
zuwa haskensa mai banmamaki. 10 Dā ku ba mutane ba ne, amma yanzu ku mutanen
Allah ne; Dā ba ku karɓi jinƙai ba, amma yanzu kun karɓi jinƙai.
11 Abokaina ƙaunatattu, ina roƙonku, a matsayin bare da kuma baƙi a duniya, ku
rabu da sha'awace-sha'awacen zunubin da suke yaƙi da ranku. 12 Ku yi irin rayuwa
mai kyau a cikin masu bautar gumaka, yadda ko da sun zarge ku da yin laifi, za su
iya ganin ayyukanku nagari, su ɗaukaka Allah a ranar da zai ziyarce mu.

### *Biyayya ga masu mulki da iyayengiji*

13 Saboda Ubangiji, ku yi biyayya ga kowace hukumar da aka kafa cikin mutane,
ko ga sarki, a matsayi wanda ya fi iko, 14 ko ga gwamnoni, waɗanda ya aika domin
su hukunta masu laifi su kuma yabi masu aikata abin da yake daidai. 15 Gama nufin

† **1:25** Ish 40.6-8 * **2:6** Ish 28.16 † **2:7** Zab 118.22 ‡ **2:8** Ish 8.14

Allah ne cewa ta wurin yin nagarta za ku toshe jahilcin marasa azanci. 16 Ku yi
rayuwa kamar mutanen da aka ʼyantar, sai dai kada ku yi amfani da ʼyancinku a
matsayin hujjar aikata mugunta; ku yi rayuwa kamar bayin Allah. 17 Ku nuna ladabin
da ya dace ga kowa. Ku ƙaunaci ʼyanʼuwantakar masu bi, ku ji tsoron Allah, ku
girmama sarki.
18 Bayi, ku yi biyayya ga iyayengijinku da matuƙar ladabi, ba kawai ga waɗanda
suke da kirki da masu sauƙinkai ba, amma har ga masu zafin rai ma. 19 Gama abin
yabo ne in mutum ya yi haƙuri cikin zafin wahalar rashin adalci saboda yana sane
da Allah. 20 Amma ina abin taƙama in kuka sha duka saboda kun yi laifi kuka kuma
jimre? Sai dai in kuka sha wahala saboda yin nagari kuka kuma jimre, abin yabo ne
a gaban Allah. 21 Ga wannan ne aka kira ku, domin Kiristi ya sha wahala dominku,
ya bar muku gurbin da ya kamata ku bi.
22 "Bai taɓa yin laifi ba sam,
ba a kuma sami ƙarya a bakinsa ba."§
23 Saʼad da suka zazzage shi, bai rama ba; saʼad da ya sha wahala, bai yi barazana
ba. A maimakon haka, ya miƙa kansa ga wanda yake shariʼar adalci. 24 Shi kansa ya
ɗauki zunubanmu a jikinsa a kan itace, domin mu mutu ga zunubai mu kuma rayu
ga adalci; ta wurin raunukansa ne kuka sami warkarwa. 25 Gama dā kuna kama da
tumakin da suka ɓace, amma yanzu kun dawo ga Makiyayi da kuma Mai lura da
rayukanku.

# 3

*Matan aure da mazan Aure*

1 Haka ma, ku matan aure, ku yi biyayya ga mazanku, domin in waɗansunsu ba
su gaskata maganar ba, wataƙila a shawo kansu ba tare da magana ba 2 saʼad da
suka ga rayuwarku mai tsabta da kuma na ladabi. 3 Kyanku bai kamata yă zama na
adon jiki ba, kamar kitso da sa kayan ado na zinariya da kuma sa kaya masu tsada.
4 Maimakon haka, kyanku ya kamata yă zama ainihi na halinku na ciki, kyan da ba
ya koɗewa na tawaliʼu da kuma na natsattsen ruhu, wanda yake mai daraja a gaban
Allah. 5 Gama haka matan masu tsarki na dā waɗanda suka sa begensu ga Allah suka
yi wa kansu ado. Sun yi wa mazansu biyayya, 6 kamar Saratu, wadda ta yi biyayya
ga Ibrahim, har ta kira shi maigidanta. Ku ʼyaʼyanta ne mata in kun aikata abin da
yake daidai, ba ku kuma ba tsoro dama ba.
7 Mazan aure, ku ma, ku yi zaman sanin ya kamata yayinda kuke zama da matanku,
ku girmama su a matsayin abokan zama marasa ƙarfi da kuma a matsayin magādan
kyautar rai na alheri tare da ku, don kada wani abu yă hana adduʼoʼinku.

*Shan wahala saboda yin ayyuka alheri*

8 A ƙarshe, dukanku ku zauna lafiya da juna; ku zama masu juyayi, kuna ƙaunar
juna kamar ʼyanʼuwa, ku zama masu tausayi da kuma tawaliʼu. 9 Kada ku rama
mugunta da mugunta ko zagi da zagi, sai dai ku sa albarka, gama ga wannan ne aka
kira ku, ku kuma gāji albarka. 10 Gama,
"Duk wanda yake so yă ji daɗin rayuwa,
yă kuma ga kwanaki masu kyau
dole yă ƙame harshensa daga mugunta
leɓunansa kuma daga maganar yaudara.
11 Dole yă juye daga mugunta, ya aikata nagarta;
dole yă nemi salama yă kuma bi ta.
12 Gama idanun Ubangiji suna a kan masu adalci

§ **2:22** Ish 53.9

kunnuwansa kuma suna jin addu'arsu,
amma fuskar Ubangiji tana gāba da masu mugunta."*
13 Wa zai yi muku lahani in kun himmantu ga yin nagarta? 14 Amma ko da za ku
sha wahala saboda abin da yake daidai, ku masu albarka ne. "Kada ku ji tsoron abin
da suke tsoro; kada kuma ku firgita."† 15 Sai dai a cikin zukatanku ku keɓe Kiristi a
matsayin Ubangiji. A kullum, ku kasance a shirye ku ba da amsa ga duk wanda yake
neman ku ba da dalilin wannan begen da kuke da shi. Amma ku yi wannan cikin
tawali'u da ladabi, 16 tare da lamiri mai kyau, saboda waɗanda suke maganganun
banza a kan kyawawan ayyukanku cikin Kiristi su ji kunya da irin ɓata suna da suke
yi. 17 Ya fi kyau, in nufin Allah ne, a sha wahala don yin nagarta fiye da yin mugunta.
18 Gama Kiristi ya mutu domin zunubi sau ɗaya tak, mai adalci saboda marasa adalci,
don yă kawo ku ga Allah. An kashe shi a cikin jiki, amma an rayar da shi a Ruhu, 19 ta
wurin wanda kuma ya tafi ya yi wa ruhohin da suke a kurkuku wa'azi 20 waɗanda
dā ba su yi biyayya ba sa'ad da Allah ya jira da haƙuri a kwanaki Nuhu yayinda
ake sassaƙa jirgi. A cikinsa mutane kima ne kawai, su takwas, aka kuɓutar ta ruwa,
21 ruwan nan kuwa kwatancin baftisma ne da yanzu ya cece ku ku ma, ba kawar da
dauda daga jiki ba, sai dai yin alkawari na lamiri mai kyau ga Allah. Ya cece ku ta
wurin tashin Yesu Kiristi daga matattu, 22 wanda ya tafi sama, yana kuma a hannun
dama na Allah, mala'iku, mulkoki da kuma masu iko suna masa biyayya.

# 4

*Rayuwa saboda Allah*

1 Saboda haka, da yake Kiristi ya sha wahala a jikinsa, sai ku ma ku yi wa kanku
ɗamara da irin wannan hali, gama wanda ya sha wahala a jikinsa ya gama da zunubi
ke nan. 2 Ta haka, ba ya sauran rayuwarsa a kan mugayen sha'awace-sha'awacen
jiki, sai dai nufin Allah. 3 Gama kun ɓata lokaci sosai a dā kuna yin abubuwan da
masu bauta gumaka suka zaɓa su yi, kuna rayuwa cikin lalata, sha'awace-sha'awace,
buguwa, shashanci, shaye-shaye da kuma bautar gumaka masu banƙyama. 4 Sun yi
mamaki da ba kwa haɗa kai da su a yanzu, da ba kwa kutsa kai tare da su cikin irin
rayuwar banzan nan, har suna zaginku. 5 Amma dole su ba da lissafi gare shi wanda
yake a shirye yă shari'anta masu rai da matattu. 6 Dalilin ke nan da ya sa aka yi
wa'azin bishara har ga waɗanda yanzu suke mutattu, don ko da yake an hukunta su
a matsayin mutane a batun jiki, amma su rayu ga Allah a batun ruhu.
7 Karshen abubuwa duka ya yi kusa. Saboda haka ku kasance masu tunani mai
kyau da masu kamunkai don ku iya yin addu'a. 8 Fiye da kome, ku ƙaunaci juna
sosai, domin ƙauna tana rufe zunubai masu ɗumbun yawa. 9 Ku riƙa karɓar juna ba
da gunaguni ba. 10 Kowa yă yi amfani da kowace baiwar da ya samu don kyautata wa
waɗansu, cikin aminci yana aikata alherin Allah a hanyoyi dabam-dabam. 11 In wani
ya yi magana, ya kamata yă yi ta a matsayin wanda yake magana ainihin kalmomin
Allah. In wani yana yin hidima, ya kamata yă yi ta da ƙarfin da Allah ya tanadar,
domin a cikin kome a yabi Allah ta wurin Yesu Kiristi. A gare shi ɗaukaka da iko sun
tabbata har abada abadin. Amin.

*Shan wahala don zaman Kirista*

12 Abokaina ƙaunatattu, kada ku yi mamakin gwaji mai tsananin da kuke sha, sai
ka ce wani baƙon abu ne yake faruwa da ku. 13 Sai dai ku yi murna cewa kuna
tarayya cikin shan wahalolin Kiristi, domin ku kai ga farin ciki mai yawa sa'ad da
aka bayyana ɗaukakarsa. 14 In an zage ku saboda sunan Kiristi, ku masu albarka ne,
gama Ruhun ɗaukaka da kuma na Allah yana bisanku. 15 In kuna shan wahala, kada

* **3:12** Zab 34.12-16 † **3:14** Ish 8.12

yă zama don ku masu kisankai ne ko ɓarayi ko masu wani irin laifi ko kuma masu
shisshigi. 16 Amma fa, in kuka sha wahala a matsayin ku Kirista ne, kada ku ji kunya,
sai dai ku yabi Allah cewa kuna amsa wannan suna. 17 Gama lokaci ya yi da za a fara
yi wa iyalin Allah shari'a; in kuwa ya fara da mu, to, me zai faru da waɗanda ba sa
biyayya da bisharar Allah? 18 Kuma,
"In da ƙyar masu adalci su kuɓuta,
me zai faru da marasa tsoron Allah da kuma masu zunubi?"*
19 Saboda haka, waɗanda suke shan wahala bisa ga nufin Allah ya kamata su danƙa
kansu ga Mahaliccinsu mai aminci, su kuma ci gaba da aikata abin da yake daidai.

# 5

### *Zuwa ga dattawa da kuma samari*

1 Zuwa ga dattawan da suke cikinku, ina roƙo a matsayin ɗan'uwanku dattijo,
mashaidin shan wahalar Kiristi wanda kuma shi ma zai sami rabo cikin ɗaukakar da
za a bayyana. 2 Ku zama makiyayan garken Allah da yake a ƙarƙashin kulawarku,
kuna hidima kamar masu kula, ba kan dole ba, sai dai da yardar rai, yadda Allah yake
so ku zama; ban da kwaɗayin kuɗi, sai dai marmarin yin hidima; 3 ban da nuna iko
a kan waɗanda aka danƙa muku amana, sai dai ku zama gurbi ga garken. 4 Sa'ad da
kuwa Babban Makiyayin ya bayyana, za ku karɓi rawanin ɗaukaka marar koɗewa.
5 Samari, ku ma, ku yi biyayya ga waɗanda suka girme ku. Dukanku, ku yafa
sauƙinkai ga juna, domin,
"Allah yana gāba da mai girman kai,
amma yakan yi alheri ga mai sauƙinkai."*
6 Saboda haka, ku ƙasƙantar da kanku a ƙarƙashin hannun Allah mai ƙarfi, don yă
ɗaukaka ku a lokacin da ya ga dama. 7 Ku danƙa masa dukan damuwarku, domin
shi ne yake lura da ku.
8 Ku zama masu kamunkai, ku kuma zauna a faɗake. Abokin gābanku, Iblis yana
kewayewa kamar zaki mai ruri, yana neman wanda zai cinye. 9 Ku yi tsayayya da
shi, kuna tsayawa daram cikin bangaskiya, domin kun san cewa 'yan'uwanku ko'ina
a duniya suna shan irin wahalolin nan.
10 Allah mai dukan alheri, wanda ya kira ku ga madawwamiyar ɗaukaka cikin
Kiristi, bayan kun sha wahala na ɗan lokaci, shi da kansa zai raya ku, yă kuma sa ku
yi ƙarfi, ku kahu, ku kuma tsaya daram. 11 Gare shi bari iko yă tabbata har abada
abadin. Amin.

### *Gaisuwar ƙarshe*

12 Da taimakon Sila, wanda na ɗauka a matsayin ɗan'uwa mai aminci, na rubuta
muku a taƙaice, ina ƙarfafa ku ina kuma shaida muku cewa wannan shi ne alherin
Allah na gaske. Ku tsaya daram a cikinsa.

13 Ita wadda take a Babilon, zaɓaɓɓiya tare da ku, tana gaishe ku, haka ma ɗana
Markus.
14 Ku gai da juna da sumbar ƙauna.

Salama gare ku duka da kuke cikin Kiristi.

* **4:18** K Mag 11.31 * **5:5** K Mag 3.34

# 2 Bitrus

1 Siman Bitrus, bawa da kuma manzon Yesu Kiristi,

Zuwa ga waɗanda ta wurin adalcin Allahnmu da Mai Cetonmu Yesu Kiristi sun sami bangaskiya mai daraja irin tamu.

2 Alheri da salama su zama naku a yalwace ta wurin sanin Allah da Yesu Ubangijinmu.

### *Mai da kira da kuma zaɓen da aka wa mutum yă zama tabbatacce*

3 Ikonsa na Allahntaka ya ba mu kome da muke bukata don rayuwa da kuma tsoron
Allah ta wurin sanin wanda ya kira mu ta wurin ɗaukakarsa da nagartarsa. 4 Ta
wurin waɗannan ya ba mu alkawaransa masu girma da kuma masu daraja, domin
ta wurinsu ku iya yin tarayya cikin Allahntakarsa, ku kuma kuɓuta daga lalatar da
take cikin duniya wadda mugayen sha'awace-sha'awace suke jawowa.
5 Saboda haka, ku yi iyakar ƙoƙari ku ƙara wa bangaskiyarku nagarta; ga nagarta
kuwa, ku ƙara mata sani; 6 ga sani kuma ku ƙara masa kamunkai; ga kamunkai
kuma ku ƙara da daurewa; ga daurewa kuwa ku ƙara da tsoron Allah; 7 ga tsoron
Allah kuma ku ƙara da nuna alheri ga 'yan'uwa; ga nuna alheri ga 'yan'uwa kuma
ku ƙara da ƙauna. 8 Domin in kuna ƙaruwa a waɗannan halaye, za su kāre ku daga
rashin tasiri da rayuwa na rashin amfani cikin saninku na Ubangijinmu Yesu Kiristi.
9 Amma in wani ba shi da su, ba shi da hangen nesa ke nan kuma makaho ne, ya
kuma manta cewa an tsarkake shi daga zunubansa na dā.
10 Saboda haka 'yan'uwana, ku ƙara aniya wajen tabbatar da kiranku da zaɓenku
da aka yi. Gama in kuka yi waɗannan abubuwa, ba za ku taɓa fāɗuwa ba, 11 za ku
sami kyakkyawar marabta cikin madawwamin mulkin Ubangijinmu da Mai Cetonmu
Yesu Kiristi.

### *Annabcin nassi*

12 Saboda haka kullum zan tuna muku da waɗannan, ko da yake kun sansu kun
kuma kahu ƙwarai cikin gaskiyar da kuke da ita yanzu. 13 A ganina ya dace in tunashe
ku muddin ina raye cikin tentin wannan jiki, 14 domin na sani na kusa in ajiye shi a
gefe, yadda Ubangijinmu Yesu Kiristi ya nuna mini a sarari. 15 Zan kuwa yi iyakacin
ƙoƙari in ga cewa bayan rabuwata kullum za ku iya tuna da waɗannan abubuwa.
16 Ba mu bi tatsuniyoyin da aka ƙaga da wayo sa'ad da muka gaya muku game da
ikon Ubangijinmu Yesu Kiristi da zuwansa ba, sai dai mu shaidu ne na ɗaukakarsa
mai girma da muka gani da ido. 17 Gama ya sami girma da ɗaukaka daga Allah
Uba sa'ad da murya ta zo masa daga Mafificiyar Ɗaukaka cewa, "Wannan Ɗana ne,
wanda nake ƙauna; da shi nake jin daɗi ƙwarai."* 18 Mu kanmu mun ji wannan
muryar da ta zo daga sama sa'ad da muke tare da shi a kan dutse mai tsarki.
19 Muna kuwa da maganar annabawa da aka ƙara tabbatar mana, zai fi kyau in
kuka lura da ita, kamar hasken da yake haskakawa a wuri mai duhu, har yă zuwa
wayewar gari da kuma haskakawar tauraron asubahi a zukatanku. 20 Gaba da kome
dai, dole ku gane cewa babu annabcin Nassin da ya fito daga fassarar annabi da
kansa. 21 Gama annabci bai taɓa samo tushensa daga nufin mutum ba, sai dai mutane
sun yi magana daga Allah yayinda Ruhu Mai Tsarki ya bishe su.

* **1:17** Mat 17.5; Mar 9.7; Luk 9.35

# 2

*Malaman ƙarya da kuma hallakarsu*

1 Amma a dā akwai annabawan ƙarya a cikin mutane, kamar yadda za a sami
malaman ƙarya a cikinku. A ɓoye za su shigar da karkataccen koyarwa mai hallaka,
har ma su yi mūsun Ubangiji mai iko duka wanda ya saye su suna kawo wa kansu
hallaka farat ɗaya. 2 Da yawa za su bi hanyoyinsu na rashin kunya su kuma sa a
rena hanyar gaskiya. 3 Cikin kwaɗayinsu waɗannan malaman ƙarya za su cuce ku
da tatsuniyoyin da suka ƙaga. Hukuncinsu yana a rataye a kansu tun da daɗewa,
hallakarsu kuma ba ta barci.
4 Gama in har Allah bai ƙyale mala'iku sa'ad da suka yi zunubi ba, amma ya tura
su cikin lahira, domin a tsare su don hukunci; 5 in har bai ƙyale duniya ta dā ba sa'ad
da ya kawo ambaliya a kan mutanenta marasa tsoron Allah, amma ya kiyaye Nuhu,
mai wa'azin adalci, da kuma waɗansu bakwai; 6 in har ya hukunta biranen Sodom da
Gomorra ta wurin ƙone su suka zama toka, ya kuma maishe su misali na abin da zai
faru da marasa tsoron Allah; 7 in kuwa har ya ceci Lot, mai adalci, wanda ya damu
ainun da ƙazamar rayuwar mutane marasa bin doka; 8 (adon kuwa abin da adalin
nan ya yi, ya kuma gani, sa'ad da yake a cikinsu, sai kowace rana yakan ji ciwon
aikinsu na kangara a zuciyarsa mai adalci) 9 in haka ne, to, Ubangiji ya san yadda
zai ceci mutane masu tsoron Allah daga gwaje-gwaje, yǎ kuma tsare marasa adalci
don ranar hukunci, har yǎ zuwa ranar shari'a. 10 Wannan gaskiya ce musamman
ga waɗanda suke bin sha'awace-sha'awacen lalaci na mutuntaka, suna kuma rena
masu mulki.
Da ƙarfin hali da kuma girman kai, waɗannan mutane ba sa tsoro kawo zargin ɓata
sunan talikan sama; 11 duk da haka ko mala'iku ma da suka fi su ƙarfi suka kuma
fi su iko, ba sa kawo irin wannan zargi na ɓata suna game da waɗannan talikai a
gaban Ubangiji. 12 Amma waɗannan mutane suna yin saɓo a kan abubuwan da ba
su fahimta ba. Suna kama da dabbobi marasa hankali, halittun da suke bin abin da
jikinsu ya faɗa musu kawai, waɗanda aka haifa don a kama a hallaka, kuma kamar
dabbobi su ma za su hallaka.
13 Za a yi musu sakamako da muguntar da suka yi. A ra'ayinsu jin daɗi shi ne a
yi annashuwa da rana tsaka. Su ƙazamai ne marasa kunya, suna cike da jin daɗin
sha'awace-sha'awacensu yayinda suke cin biki tare da ku. 14 Idanunsu sun cike da
zina, ba sa ƙoshi da yin zunubi; suna jarrabtar waɗanda ba tsayayyu ba; gwanaye
ne a kan kwaɗayi, la'anannun iri! 15 Sun bar miƙaƙƙiyar hanya suka bauɗe suna
bin hanyar Bala'am ɗan Beyor, wanda ya yi ƙaunar hakkin mugunta. 16 Amma an
tsawata masa saboda laifinsa ta wurin jaki, dabbar da ba ta magana, wadda ta yi
magana da muryar mutum ta kuma kwaɓi haukan annabin.
17 Waɗannan mutane maɓulɓulai ne babu ruwa da kuma hazon da guguwar iska
take kora. An shirya matsanancin duhu dominsu. 18 Gama suna surutai banza na
girman kai, ta wurin son bin fasikanci na mutuntaka, sukan jan hankulan mutanen
da suke kuɓucewa daga waɗancan masu zama cikin kuskure. 19 Suna yin musu
alkawarin 'yanci, yayinda su kansu bayi ne ga aikin lalata gama mutum bawa ne
ga duk abin da ya mallake shi. 20 In har sun kuɓuta daga lalacin duniya ta wurin
sanin Ubangijinmu da kuma Mai Cetonmu Yesu Kiristi sai suka sāke koma a cikin
lalacin, har ya rinjaye su, za su fi muni a ƙarshe fiye da farko. 21 Zai fi musu kyau da
ba su taɓa sanin hanyar adalci ba, fiye da a ce sun sani sa'an nan su juya bayansu
ga umarni mai tsarkin nan da aka ba su. 22 A kansu karin maganan nan gaskiya
ce, "Kare ya koma kan amansa,"* da kuma, "Alade da aka yi wa wanka, ya koma
birgimarsa cikin laka."

* **2:22** K Mag 26.11

# 3

*Ranar Ubangiji*

1 Abokaina ƙaunatattu, wannan ita ce wasiƙata ta biyu gare ku. Na rubuta su
biyun su zama abin tuni don su faɗakar da ku ga tunani mai kyau. 2 Ina so ku
tuna da kalmomin da annabawa masu tsarki na dā suka faɗa da kuma umarnin da
Ubangijinmu da Mai Cetonmu ya bayar ta wurin manzanninku.
3 Da farko dai, dole ku fahimci wannan cewa a kwanakin ƙarshe masu ba'a za su
zo suna ba'a, suna bin mugayen sha'awace-sha'awacensu. 4 Za su ce, "Ina wannan
'dawowar' da ya yi alkawari ne? Tun mutuwar kakanninmu, kome yana tafiya kamar
yadda yake tun farkon halitta." 5 Amma da gangan suke manta cewa tun dā can ta
wurin maganar Allah sammai suka kasance aka kuma yi ƙasa daga ruwa ta wurin
ruwa kuma. 6 Ta wurin waɗannan ruwan ne aka nutsar, aka kuma hallakar da duniya
ta wancan lokaci. 7 Ta wurin wannan magana ce aka ajiye sammai da ƙasa na yanzu
domin wuta, an ajiye su kuma don ranar hukunci da hallaka ta mutane marasa tsoron
Allah.
8 Amma kada ku manta da wannan abu guda ɗaya, abokaina ƙaunatattu. Ga
Ubangiji kwana ɗaya kamar shekaru dubu ne, shekaru dubu kuma kamar kwana
ɗaya ne. 9 Ubangiji ba mai jinkiri ba ne wajen cika alkawarinsa, yadda waɗansunku
suka fahimci jinkiri. Yana haƙuri da ku, ba ya so wani yǎ hallaka, sai dai kowa yǎ
kai ga tuba.
10 Amma ranar Ubangiji za tǎ zo kamar ɓarawo. Sammai za su ɓace da ruri,
abubuwan da suke cikinsu za su ƙone, ƙasa kuma da dukan abin da yake cikinta
za su tonu.
11 Da yake za a hallaka dukan abubuwa ta haka, waɗanne irin mutane ne ya kamata
ku zama? Ya kamata ku yi rayuwar tsarki da ta tsoron Allah, 12 yayinda kuke zuba
ido ga zuwan ranar Allah kuna gaggauta zuwanta. Wannan rana za tǎ kawo wa
sammai hallaka ta ƙunan wuta, abubuwa kuma za su narke don zafi. 13 Amma bisa
ga alkawarinsa muna zuba ido ga sabuwar sama da kuma sabuwar ƙasa, inda adalci
zai yi zama.
14 Saboda haka, abokaina ƙaunatattu, da yake kuna zuba ido ga wannan, sai ku yi
matuƙar ƙoƙari don a same ku ba tabo, sai dai zaman salama da shi. 15 Ku yi zaman
sanin cewa haƙurin Ubangijinmu yana nufin ceto ne, kamar yadda ƙaunataccen
ɗan'uwanmu Bulus ma ya rubuta muku da hikimar da Allah ya ba shi. 16 Haka yake
rubutu cikin dukan wasiƙunsa, yana magana a cikinsu a kan waɗannan al'amura.
Wasiƙunsa sun ƙunshi waɗansu abubuwa masu wuyar fahimta, waɗanda jahilai da
kuma waɗanda ba tsayayyu ba ne suke murɗe ma'anarsu, kamar yadda suke yi da
sauran Nassosi, ta haka suke jawo wa kansu hallaka.
17 Saboda haka, abokaina ƙaunatattu, da yake kun riga kun san wannan, sai ku
zauna a faɗake don kada a ɗauke hankalinku ta wurin kuskuren marasa bin dokan
nan har ku fāɗi daga matsayinku. 18 Sai dai ku yi girma cikin alheri da sanin
Ubangijinmu da Mai Cetonmu Yesu Kiristi.

A gare shi ɗaukaka ta tabbata yanzu da har abada! Amin.

# 1 Yohanna

*Kalman da ya zama mutum*

1 Wannan da ya kasance tun farko, wanda muka ji, wanda muka gani da idanunmu,
wanda muka duba, hannuwanmu kuma suka taɓa, wannan ne muke shela game da
Kalman rai. 2 Wannan Rai ya bayyana, muka kuwa gan shi, muka kuma shaida shi,
muna kuwa yin muku shelar wannan rai madawwami, wanda dā yake tare da Uba,
ya kuma bayyana a gare mu. 3 Muna yin muku shelar abin da muka gani, muka
kuma ji ne, domin ku ma ku yi zumunci tare da mu. Zumuncinmu kuwa yana tare
da Uba da kuma Ɗansa, Yesu Kiristi. 4 Muna rubuta wannan domin farin cikinmu
yǎ zama cikakke.

*Tafiya cikin haske*

5 Wannan shi ne saƙon da muka ji daga wurinsa, muna kuma sanar da ku cewa
Allah haske ne; a cikinsa kuwa babu duhu ko kaɗan. 6 In muka ce muna zumunci
da shi amma muna tafiya cikin duhu, ƙarya muke yi, kuma ba ma rayuwa bisa
ga gaskiya. 7 Amma in muna tafiya cikin haske, yadda yake cikin haske, muna da
zumunci da juna ke nan, kuma jinin Yesu, Ɗansa, yana tsarkake mu daga dukan[*]
zunubi.
8 In muka ce ba mu da zunubi, muna ruɗin kanmu ne, gaskiya kuwa ba ta cikinmu.
9 In muka furta zunubanmu, shi mai aminci ne, mai adalci kuma, zai gafarta mana
zunubanmu, yǎ kuma tsarkake mu daga dukan rashin adalci. 10 In muka ce ba mu
yi zunubi ba, mun mai da shi maƙaryaci ke nan, maganarsa kuwa ba ta da wuri a
cikinmu.

## 2

1 'Ya'yana ƙaunatattu, ina rubuta muku wannan ne don kada ku yi zunubi. Amma
in wani ya yi zunubi, muna da wani wanda yake magana da Uba don taimakonmu,
wato, Yesu Kiristi, Mai Adalci. 2 Shi ne hadayar kafara saboda zunubanmu, kuma ba
don namu kaɗai ba amma har ma da zunuban duniya duka.
3 Ta haka za mu tabbata cewa mun san shi in muna yin biyayya da umarnansa.
4 Mutumin da ya ce, "Na san shi," amma ba ya yin abin da ya umarta, maƙaryaci
ne, gaskiya kuwa ba ta cikinsa. 5 Amma in wani ya yi biyayya da maganarsa, ƙaunar
Allah ta zama cikakkiya ke nan a cikinsa. Ta haka muka san cewa muna cikinsa.
6 Duk wanda ya ce yana rayuwa a cikinsa dole yǎ yi tafiya kamar yadda Yesu ya yi.
7 Abokaina ƙaunatattu, ba sabon umarni nake rubuta muku ba, a'a, daɗaɗɗen
umarnin nan ne, wanda kuke da shi tun farko. Wannan tsohon umarni shi ne saƙon
da kuka riga kuka ji. 8 Duk da haka ina rubuta muku sabon umarni; ana ganin
gaskiyar umarnin a cikinsa da kuma cikinku, gama duhu yana shuɗewa, haske na
gaskiya kuwa yana haskakawa.
9 Duk wanda ya ce yana cikin haske yana kuma ƙin ɗan'uwansa, ashe a duhu yake
har yanzu. 10 Duk wanda yake ƙaunar ɗan'uwansa, a cikin hasken yake rayuwa ke
nan, kuma babu wani abin da yake cikinsa da zai sa yǎ yi tuntuɓe. 11 Amma duk
wanda yake ƙin ɗan'uwansa, cikin duhu yake, yana kuma tafiya cikin duhu ke nan;
bai ma san inda za shi ba, domin duhun ya makanta shi.
12 Ina rubuta muku, 'ya'yana ƙaunatattu,
domin an gafarta muku zunubanku saboda sunansa.
13 Ina rubuta muku, ubanni,

* **1:7** Ko kuwa kowane

domin kun san shi wanda yake tun farko.
Ina rubuta muku, samari,
domin kun ci nasara a kan mugun nan.

14 Ina rubuta muku, ʼyaʼyana ƙaunatattu,
domin kun san Uba.
Ina rubuta muku, ubanni,
domin kun san shi wanda yake tun farko.
Ina rubuta muku, samari,
domin kuna da ƙarfi,
maganar Allah kuwa tana zaune a cikinku,
kun kuma ci nasara a kan mugun nan.

### *Kada ku ƙaunaci duniya*

15 Kada ku ƙaunaci duniya, ko wani abin da yake cikinta. In wani yana ƙaunar
duniya, ƙaunar Uba ba ta cikinsa. 16 Gama duk abin da yake na duniya, kamar
shaʼawace-shaʼawacen mutuntaka, shaʼawar idanunsa, da kuma taƙama da abin da
yake da shi, yake kuma yi, ba daga wurin Uba suke fitowa ba sai dai daga duniya.
17 Duniya da shaʼawace-shaʼawacenta suna shuɗewa, amma mutumin da yake aikata
nufin Allah, zai rayu har abada.

### *Gargaɗi a kan magabcin Kiristi*

18 ʼYaʼyana ƙaunatattu, waɗannan su ne kwanakin ƙarshe; kuma kamar yadda
kuka ji cewa magabcin Kiristi yana zuwa, ko yanzu ma abokan gāban Kiristi da yawa
sun zo. Ta haka muka san cewa kwanakin ƙarshe sun iso. 19 Waɗannan masu gāba
da Kiristi suna cikinmu a dā, amma sun bar mu, don tun dā ma su ba namu ba ne.
Ai, da su namu ne, da har yanzu suna tare da mu. Amma sun bar mu, wannan ya
nuna a fili cewa su ba namu ba ne.
20 Amma ku kam, kuna da shafewa daga wurin Mai Tsarkin nan, kuma dukanku
kun san gaskiya. 21 Ina rubuta muku ba domin ba ku san gaskiya ba ne, aʼa, sai
dai domin kun santa, kun kuma san cewa babu yadda ƙarya za tă fito daga gaskiya.
22 Wane ne maƙaryaci? Ai, shi ne mutumin da yake mūsun cewa Yesu shi ne Kiristi.
Irin wannan mutum shi ne magabcin Kiristi, ya yi mūsun Uban da kuma Ɗan. 23 Ba
wanda yake mūsun Ɗan, saʼan nan yă ce yana da Uban; duk wanda ya yarda da Ɗan,
yana da Uban a cikinsa ke nan.
24 Ku lura fa cewa abin da kuka ji daga farko, bari yă ci gaba da kasance a cikinku.
In kuwa ya ci gaba da zama a cikinku, za ku kasance a cikin Ɗan, da kuma a cikin
Uban. 25 Wannan shi ne abin da ya yi mana alkawari, wato, rai madawwami.
26 Ina rubuta muku waɗannan abubuwa ne game da waɗanda suke ƙoƙari su sa
ku kauce. 27 Game da ku kuwa, shafan nan da kuka karɓa daga gare shi tana nan
a cikinku, ba kwa kuma bukata wani yă koyar da ku. Amma kamar yadda shafan
nan tasa tana koya muku kome, ita kuwa gaskiya ce ba ƙarya ba, yadda dai ta koya
muku, to, sai ku zauna a cikinsa.

### *ʼYaʼyan Allah*

28 Yanzu fa, ya ku ʼyaʼyana ƙaunatattu, sai ku ci gaba a cikinsa, domin saʼad da ya
bayyana, mu iya tsaya gabagadi babu kunya a dawowarsa.
29 In kun san cewa shi mai adalci ne, to, kun dai san cewa duk mai aikata abin da
yake daidai haifaffensa ne.

## 3

1 Dubi irin ƙaunar da Uba ya ƙaunace mu da ita mana, har ana ce da mu ʼyaʼyan
Allah! Haka kuwa muke! Dalilin da ya sa duniya ba tă san mu ba shi ne, don ba tă

san shi ba. 2 Abokaina ƙaunatattu, yanzu, mu 'ya'yan Allah ne, kuma abin da za mu
zama nan gaba ba a riga an bayyana ba. Sai dai mun san cewa sa'ad da Kiristi ya
bayyana, za mu zama kamar sa, domin za mu gan shi kamar yadda yake. 3 Duk mai
wannan bege a cikinsa yakan tsarkake kansa, kamar yadda shi Kiristi yake da tsabta.
4 Duk mai yin zunubi yana karya doka ne; tabbatacce, zunubi, karya doka ne. 5 Sai
dai kun san cewa Kiristi ya bayyana ne domin yă ɗauke zunubanmu. A cikinsa kuwa
babu zunubi. 6 Ba mai rayuwa a cikinsa da yake cin gaba da yin zunubi. Kowa da
yake aikata zunubi, bai taɓa ganinsa ba, bai ma san shi ba.
7 'Ya'yana ƙaunatattu, kada ku yarda wani yă ruɗe ku. Duk mai yin abin da yake
daidai mai adalci ne, yadda Kiristi yake mai adalci. 8 Duk mai aikata abin da yake
zunubi shi na Iblis ne, domin Iblis mai aikata zunubi ne tun farko. Dalilin da ya sa
Ɗan Allah ya bayyana kuwa shi ne don yă rushe aikin Iblis. 9 Babu haifaffe na Allah
da zai ci gaba da yin zunubi, domin iri na Allah yana a cikinsa; ba zai iya ci gaba
da yin zunubi ba, domin haifaffe ne na Allah. 10 Ta haka muka san waɗanda suke
'ya'yan Allah da kuma waɗanda suke 'ya'yan Iblis. Duk wanda ba ya yin abin da
yake daidai, ba ɗan Allah ba ne; haka ma wanda ba ya ƙaunar ɗan'uwansa.

### *Ku ƙaunaci juna*

11 Wannan shi ne saƙon da kuka ji tun farko. Ya kamata mu ƙaunaci juna. 12 Kada
ku zama kamar Kayinu, wanda ya zama na mugun nan, ya kuma kashe ɗan'uwansa.
Me ya sa ya kashe shi? Domin ayyukansa mugaye ne, na ɗan'uwansa kuma na adalci
ne. 13 Kada ku yi mamaki 'yan'uwana, in duniya ta ƙi ku. 14 Mun san cewa mun riga
mun ratsa daga mutuwa zuwa rai, domin muna ƙaunar 'yan'uwanmu. Duk wanda
ba ya ƙauna matacce ne har yanzu. 15 Duk mai ƙin ɗan'uwansa mai kisankai ne, kun
kuma san cewa ba mai kisankan da yake da rai madawwami a cikinsa.
16 Yadda muka san ƙauna ke nan, wato, Yesu Kiristi ya ba da ransa dominmu.
Ya kamata mu ma mu ba da rayukanmu domin 'yan'uwanmu. 17 In wani yana da
arziki, ya kuma ga ɗan'uwansa cikin rashi, bai kuwa taimake shi ba, anya, ƙaunar
Allah tana a cikinsa kuwa? 18 'Ya'yana ƙaunatattu, kada mu yi ƙauna da fatar baki
kawai, sai dai mu nuna ta ta wurin aikatawa da kuma gaskiya.
19 Ta haka muka san cewa mu na gaskiya ne, kuma za mu iya tsaya a gaban Allah
ba tare da rawar jiki ba. 20 Idan zuciyarmu ta nuna mana muna da laifi, mun san
cewa Allah ya fi zuciyarmu, ya kuma san dukan kome. 21 Abokaina ƙaunatattu, in
zukatanmu ba su ba mu laifi ba, muna da ƙarfin halin tsayawa a gaban Allah ke nan.
22 Muna kuma samun dukan abin da muka roƙa daga gare shi, domin muna biyayya
da umarnansa, muna kuma yin abin da ya gamshe shi. 23 Umarninsa kuwa shi ne,
mu gaskata da sunan Ɗansa, Yesu Kiristi, mu kuma ƙaunaci juna kamar yadda ya
umarce mu. 24 Waɗanda suke biyayya da umarnansa kuwa suna rayuwa a cikinsa,
shi kuma a cikinsu. Ta haka muka san cewa yana raye a cikinmu. Mun san haka ta
wurin Ruhun da ya ba mu.

## 4

### *Gwada ruhohi*

1 Abokaina ƙaunatattu, ba kowane ruhu za ku gaskata ba, sai dai ku gwada ruhohi
don ku ga ko daga Allah ne, domin annabawan ƙarya da yawa sun fito duniya. 2 Ga
yadda za ku gane Ruhun Allah, duk ruhun da ya yarda cewa Yesu Kiristi ya zo cikin
jiki, to, daga Allah yake. 3 Amma duk ruhun da bai yarda da Yesu ba, ba daga Allah
ba ne, ruhun magabcin Kiristi ne, wanda kuka ji yana zuwa, har ma ya riga ya shigo
duniya.

4 Ku, 'ya'yana ƙaunatattu, ku daga Allah ne, kun kuma yi nasara a kan magabtan
Kiristi, domin wanda yake a cikinku ya fi wanda yake a duniya girma. 5 Su daga
duniya ne saboda haka suke magana yadda duniya take ganin abubuwa, duniya kuwa
tana sauraronsu. 6 Mu daga Allah ne, kuma duk wanda ya san Allah yakan saurare
mu. Amma duk wanda ba daga Allah ba, ba ya sauraronmu. Ta haka ne muke gane
Ruhun gaskiya, da kuma ruhun ƙarya.

### *Kaunar Allah da kuma tamu*

7 Abokaina ƙaunatattu, mu ƙaunaci juna, domin ƙauna tana zuwa daga Allah ne.
Duk mai ƙauna, haifaffe ne na Allah, ya kuma san Allah. 8 Duk wanda ba ya ƙauna,
bai san Allah ba, domin Allah ƙauna ne. 9 Ga yadda Allah ya nuna ƙaunarsa a
cikinmu, Allah ya aiki makaɗaici Ɗansa zuwa duniya domin mu rayu ta wurinsa.
10 Wannan ita ce ƙauna, wato, ba mu ne muka ƙaunaci Allah ba, sai dai shi ne ya
ƙaunace mu, ya kuma aiko Ɗansa yă zama hadaya ta kafara saboda zunubanmu.
11 Abokaina ƙaunatattu, da yake Allah ya ƙaunace mu haka, ya kamata mu ma mu
ƙaunaci juna. 12 Ba wanda ya taɓa ganin Allah; amma in muna ƙaunar juna, Allah
yana raye a cikinmu, ƙaunarsa kuwa ta zama cikakkiya a cikinmu ke nan.
13 Mun san cewa muna rayuwa a cikinsa shi kuma a cikinmu, domin ya ba mu
Ruhunsa. 14 Mun gani, mun kuma shaida cewa Uba ya aiko Ɗansa domin yă zama
Mai Ceton duniya. 15 Duk wanda ya yarda cewa Yesu Ɗan Allah ne, Allah yana raye a
cikinsa, shi kuma a cikin Allah. 16 Ta haka muka sani, muke kuma dogara ga ƙaunar
da Allah yake mana.
Allah ƙauna ne. Duk wanda yake rayuwa cikin ƙauna, yana rayuwa a cikin Allah
ne, Allah kuma a cikinsa. 17 Ta haka, ƙauna ta zama cikakkiya a cikinmu domin mu
kasance masu ƙarfin hali a ranar shari'a, domin a wannan duniya muna kama da
shi. 18 Babu tsoro cikin ƙauna. Cikakkiyar ƙauna dai takan kawar da tsoro, domin
hukunci ne yake kawo tsoro. Mai jin tsoro ba cikakke ba ne a cikin ƙauna.
19 Muna ƙauna, domin ya ƙaunace mu da farko. 20 Duk wanda ya ce, "Ina ƙaunar
Allah," amma yana ƙin ɗan'uwansa, maƙaryaci ne. Gama duk wanda ba ya ƙaunar
ɗan'uwansa da yake gani, ba zai iya ƙaunar Allah wanda ba ya gani ba. 21 Ya
kuma ba mu wannan umarni cewa duk wanda yake ƙaunar Allah, dole yă ƙaunaci
ɗan'uwansa.

## 5

### *Bangaskiya cikin Ɗan Allah*

1 Kowa ya gaskata cewa Yesu shi ne Kiristi, shi haifaffe na Allah ne, kuma duk
mai ƙaunar mahaifi kuwa, yakan ƙaunaci ɗansa ma. 2 Ga yadda muka san cewa
muna ƙaunar 'ya'yan Allah. Muna yin haka ta wurin ƙaunar Allah da kuma aikata
umarnansa. 3 Kaunar Allah ita ce, a yi biyayya da umarnansa. Umarnansa kuwa
ba masu nauyi ba ne; 4 domin duk haifaffe na Allah yana cin nasara a kan duniya.
Bangaskiyarmu kuwa ita ce ta ba mu wannan nasara a kan duniya. 5 Wa ya cin
nasara a kan duniya? Sai wanda ya gaskata cewa Yesu Ɗan Allah ne.
6 Ga wanda ya zo ta wurin ruwa da jini, wato, Yesu Kiristi. Bai zo ta wurin ruwa
kaɗai ba, sai dai ta wurin ruwa da kuma jini. Ruhu ne kuwa yake ba da shaida,
gama Ruhu shi ne gaskiya. 7 Akwai shaidu uku, wato, 8 Ruhu,* da ruwa, da kuma
jini; waɗannan uku kuwa manufarsu ɗaya ce. 9 Tun da yake mukan yarda da shaida
mutane, ai, shaidar Allah ta fi ƙarfi. Wannan ita ce shaidar Allah, wato, ya shaidi

* **5:8** Rubuce-rubucen hannu na baya-bayan nan na Bulget shaida a sama: Uba, Kalma da kuma Ruhu Mai Tsarki, waɗannan uku kuwa ɗaya ne. 8 Akwai kuma uku da suka ba da shaida a duniya, wannan: Ruhu (babu kalman nan a rubuce-rubucen hannu na Girik kafin karni na goma sha shida)

Ɗansa. [10] Duk wanda ya gaskata da Ɗan Allah, yana da shaidan nan a zuciyarsa. Duk
wanda bai gaskata da Allah ba kuwa ya mai da shi maƙaryaci, domin bai gaskata
shaidar da Allah ya bayar game da Ɗansa ba. [11] Wannan kuwa ita ce shaidar; cewa
Allah ya ba mu rai madawwami, wannan rai kuwa yana cikin Ɗansa. [12] Duk wanda
yake da Ɗan, yana da rai; wanda kuwa ba shi da Ɗan Allah, ba shi da rai.

*Karshen magana*

[13] Ina rubuta waɗannan abubuwa gare ku, ku da kuka gaskata sunan Ɗan Allah
domin ku san kuna da rai madawwami. [14] Wannan shi ne ƙarfin halin da muke da
shi sa'ad da muke zuwa a gaban Allah, gama mun san cewa kome muka roƙa bisa ga
nufinsa, yakan saurare mu. [15] In kuwa muka san cewa yana sauraranmu, ko mene
ne muka roƙa, mun sani, mun riga mun sami abin da muka roƙa daga gare shi ke
nan.

[16] Kowa ya ga ɗan'uwansa yana yin zunubin da bai kai ga mutuwa ba, sai yǎ yi
masa addu'a. Ta dalilin mai addu'an nan kuwa, Allah zai ba da rai ga mai yin zunubin
da bai kai ga mutuwa ba. Akwai zunubin da yakan kai ga mutuwa. Ban ce a yi addu'a
domin wannan ba. [17] Duk rashin adalci, zunubi ne, amma akwai waɗansu zunuban
da ba sa kai ga mutuwa.

[18] Mun san cewa kowane haifaffe na Allah ba ya cin gaba da yin zunubi;
kasancewarsa haifaffe na Allah ita takan kāre shi, mugun kuwa ba zai iya cuce shi
ba. [19] Mun san cewa mu 'ya'yan Allah ne, duniya duka kuwa tana hannun Mugun.
[20] Mun san cewa Ɗan Allah ya zo duniya, ya kuma ba mu ganewa domin mu san shi
wanda yake na gaskiya. Mu kuwa muna cikinsa, shi da yake Allah na gaskiya wato,
cikin Ɗansa Yesu Kiristi. Shi ne Allah na gaskiya da kuma rai na har abada.

[21] 'Ya'yana ƙaunatattu, ku yi nesa da gumaka.

# 2 Yohanna

1 Dattijon nan,

Zuwa ga uwargida zaɓaɓɓiya da kuma ʼyaʼyanta, waɗanda nake ƙauna ƙwarai da
gaske kuma ba ni kaɗai ba, amma har da dukan waɗanda suka san gaskiya. 2 Muna
ƙaunarku saboda gaskiyan nan, wadda take cikinmu za tă kuma kasance tare da mu
har abada.

3 Alheri, jinƙai da kuma salama daga Allah Uba da kuma Yesu Kiristi, Ɗan Uba, su
kasance tare da mu cikin gaskiya da ƙauna.

4 Na yi farin ciki ƙwarai, da na sami waɗansu ʼyaʼyanki suna tafiya cikin gaskiya,
kamar yadda Uba ya umarce mu. 5 Yanzu kuma, uwargida ƙaunatacciya, ba sabon
umarni nake rubuta miki ba sai dai wanda muke da shi tun farko. Ina roƙo cewa
mu ƙaunaci juna. 6 Kauna, ita ce mu yi biyayya ga umarnansa. Kamar yadda kuka
ji tun da fari, umarninsa shi ne ku yi zaman ƙauna.
7 Masu ruɗi da yawa, waɗanda ba su yarda da zuwan Yesu Kiristi cikin jiki ba, sun
riga sun fito a duniya. Duk irin mutumin nan mai ruɗi ne kuma magabcin Kiristi.
8 Ku lura don kada ku yi hasarar aikin da kuka yi, sai dai ku sami cikakken lada. 9 Duk
mutumin da bai tsaya a kan koyarwar Kiristi ba, amma ya yi ƙari a kanta, mutumin
nan ba shi da Allah. Amma wanda ya tsaya a kan koyarwar Kiristi, yana da Uban da
kuma Ɗan. 10 Duk wanda ya zo wurinku bai kuma kawo koyarwan nan ba, kada ku
karɓe shi a gidanku ko ku marabce shi. 11 Duk wanda ya karɓe shi yana tarayya da
mugun aikinsa ke nan.

12 Ina da abubuwa da dama da zan rubuta muku, sai dai ba na so in yi amfani da
takarda da inki in rubuta. A maimako, ina fata in ziyarce ku in kuma yi magana da
ku fuska da fuska, domin farin cikinmu yă zama cikakke.

13 ʼYaʼyan ʼyarʼuwarki wadda Allah ya keɓe, suna gaishe ku.

# 3 Yohanna

1 Dattijon nan,

Zuwa ga ƙaunataccen abokina Gayus, wanda nake ƙauna ƙwarai da gaske.

2 Abokina ƙaunatacce, ina addu'a ka sami zaman lafiya don kome yǎ yi maka
daidai, kamar yadda ruhunka yake zaune lafiya. 3 Na yi farin ciki ƙwarai sa'ad da
waɗansu 'yan'uwa suka zo suka yi zance game da yadda kake da aminci ga gaskiyan
nan da kuma yadda kake cin gaba cikin gaskiyan nan. 4 Ba abin da ya fi sa ni farin
ciki fiye da in ji cewa 'ya'yana suna cikin gaskiyan nan.
5 Abokina ƙaunatacce, kana da aminci cikin abin da kake yi wa 'yan'uwa, ko da
yake su baƙi ne a gare ka. 6 Sun faɗa wa ikkilisiya game da ƙaunarka. Za ka kyauta
in ka sallame su a hanyar da ta cancanci Allah. 7 Saboda Sunan nan ne suka fito, ba
sa karɓan wani taimako daga waɗanda ba masu bi ba. 8 Saboda haka ya kamata mu
nuna halin karɓan baƙi ga irin mutanen nan domin mu yi aiki tare saboda gaskiyan
nan.
9 Na rubuta wa ikkilisiya, amma Diyotirefes, wanda yake son zama na farko, ya ƙi
yǎ yi hulɗa da mu. 10 Saboda haka in na zo, zan tone abin da yake yi, yana surutu
game da mu, yana ɓaɓɓata mu. Wannan ma bai ishe shi ba, har yana ƙin marabtar
'yan'uwa. Yana hana waɗanda suke so yin haka, yana ma korinsu daga ikkilisiya.
11 Abokina ƙaunatacce, kada ka yi koyi da abin da yake mugu sai dai abin da yake
nagari. Duk mai yin abin da yake nagari daga Allah yake. Duk mai yin abin da yake
mugu bai taɓa sanin Allah ba. 12 Demetiriyus yana da shaida mai kyau daga wurin
kowa, har gaskiya kanta ma ta shaide shi. Mu ma muna ba da shaida mai kyau a
kansa, ka kuma san cewa shaidarmu gaskiya ce.

13 Ina da abubuwa da dama da zan rubuta maka, sai dai ba na so in yi amfani da
alƙalami da inki in rubuta su. 14 Ina fata in gan ka nan ba da daɗewa ba, za mu
kuwa yi magana fuska da fuska.

15 Salama gare ka.

Abokai a nan suna gaishe ka. Ka gai da abokai a can da sunansu.

# Yahuda

1 Yahuda, bawan Yesu Kiristi, ɗan'uwan Yaƙub,

Zuwa ga waɗanda aka kira, waɗanda Allah Uba yake ƙauna, waɗanda kuma Yesu
Kiristi ya kiyaye.

2 Jinƙai, salama da kuma ƙauna, su kasance tare da ku a yalwace.

*Zunubi da hallakar marasa tsoron Allah*

3 Abokaina ƙaunatattu, ko da yake na yi marmari ƙwarai in rubuta muku game da
ceton nan namu, sai na ga ya dace in rubuta, in gargaɗe ku ku tsaya da ƙarfi cikin
bangaskiya wadda aka danƙa wa mutane masu tsarki na Allah sau ɗaya tak. 4 Na
faɗa haka ne domin waɗansu mutanen da aka rubuta hukuncinsu tun dā sun shiga
cikinku a ɓoye. Su fa marasa tsoron Allah ne. Su ne waɗanda suka mai da alherin
Allahnmu ya zama dalilin yin fasikanci, suna kuma mūsun Yesu Kiristi wanda shi ne
Makaɗaici Mai Iko Duka da kuma Ubangijinmu.
5 Ko da yake kun riga kun san duk wannan, ina so in tuna muku cewa Ubangiji ya
ceci mutanensa daga Masar, duk da haka daga baya ya hallaka waɗanda ba su ba da
gaskiya ba. 6 Haka ma mala'ikun da ba su riƙe matsayinsu na iko ba, waɗanda suka
bar ainihin mazauninsu, su ne ya tsare a duhu daure da dawwammamun sarƙoƙi
don hukunci ta babbar Ranan nan. 7 Haka ma Sodom da Gomorra da garuruwan
da suke kewaye da su, waɗanda su ma suka ba da kansu ga fasikanci da muguwar
sha'awar jiki, sun zama misalin waɗanda suke shan hukuncin madawwamiyar wuta.
8 Haka yake da masu mafarke-mafarken nan, gama sun ƙazantar da jikunansu,
suka ƙi bin masu mulki, suna ɓata sunan talikan sararin sama. 9 Kai, ko Mika'ilu
babban shugaban mala'iku ma, sa'ad da yake mūsu da Iblis game da gawar Musa,
bai yi garajen ɗora masa laifi da baƙar magana ba, sai dai ya ce, "Ubangiji yă tsawata
maka!" 10 Duk da haka mutanen nan suna maganar banza a kan kome da ba su gane
ba; kuma abubuwan da suka fahimta bisa ga jiki, kamar dabbobi marasa hankali,
waɗannan abubuwa ne suke hallaka su.
11 Kaitonsu! Gama sun kama hanyar Kayinu; sun ruga a guje garin neman riba
cikin kuskure kamar Bala'am; aka kuma hallaka su cikin tawayen Kora.
12 Waɗannan mutane sun zama kamar ƙazanta a taronku na soyayya, suna ta ciye-
ciye a cikinku, ba kunya ba tsoro. Su masu kiwo ne da suke ciyar da kansu kawai.
Su kamar hadari ne da babu ruwa da iska take kori. Su kamar itatuwa ne, marasa
'ya'ya da rani, waɗanda aka tumɓuke, ko kamar itatuwan da aka tumɓuke suka kuma
mutu ƙurmus. 13 Su kamar raƙuman ruwan teku ne masu hauka, suna taƙama da
tumbatsan kumfar kunyarsu. Su kamar taurari ne masu yawo barkatai, waɗanda
aka ajiye mugun duhu saboda su har abada.
14 Enok ma, wanda yake na bakwai daga Adamu, ya yi annabci game da waɗannan
mutane cewa, "Duba, Ubangiji yana zuwa da dubu dubban tsarkakansa 15 don yă
yi wa kowa shari'a, yă kuma hukunta duk marasa tsoron Allah game da dukan
ayyukansu na rashin tsoron Allah da suka aikata ta hanyar rashin tsoron Allah, da
kuma dukan baƙaƙen kalmomin da masu zunubi marasa tsoron Allah suka faɗa game
da shi." 16 Waɗannan mutane dai, gunaguni gare su, kullum ganin laifin waɗansu
suke yi. Muguwar sha'awa ce kaɗai tunaninsu. Sun cika da banzar magana ta yabon
kansu. Suna ruɗin mutane da zaƙin baki don samun ribar kansu.

### *Kira don jimiri*

17 Amma ku abokaina ƙaunatattu, ku tuna da abin da manzannin Ubangijinmu
Yesu Kiristi suka faɗa a dā. 18 Sun ce muku, “A kwanakin ƙarshe za a kasance
da masu ba'a waɗanda za su bi sha'awace-sha'awacensu na rashin tsoron Allah.”
19 Waɗannan mutanen ne, suke kawo rabe-rabe, masu bin abin da jiki yake so, marasa
Ruhu.
20 Amma ku, abokaina ƙaunatattu, ku gina kanku cikin bangaskiyarku mafi tsarki,
ku kuma yi addu'a cikin Ruhu Mai Tsarki. 21 Ku zauna cikin ƙaunar Allah yayinda
kuke jira jinƙan Ubangijinmu Yesu Kiristi don yă kawo ku ga rai madawwami.
22 Ku ji tausayin waɗanda suke shakka; 23 ku cece waɗansu ta wurin fizge su daga
wuta. Ga waɗansu kuma ku ji tausayinsu, amma tare da tsoro, har ma ku yi ƙyamar
tufafin da suka ɓata da ayyukansu na jiki.

### *Yabo*

24 To, yabo yă tabbata a gare shi, shi wanda yake da iko yă tsare ku daga fāɗuwa,
yă kuma miƙa ku marasa laifi a gaban ɗaukakarsa da matuƙar farin ciki. 25 Gare shi
kuma, shi da yake kaɗai Allah Mai Cetonmu, ta wurin Yesu Kiristi Ubangijinmu, bari
ɗaukaka, daraja, iko da mulki, su tabbata a gare shi, tun farkon zamanai, yanzu, da
har abada abadin! Amin.

# Ru'uya ta Yohanna

*Gabatarwa*

1 Wahayin Yesu Kiristi, wanda Allah ya ba shi yǎ nuna wa bayinsa abin da lalle
zai faru nan ba da daɗewa ba. Ya bayyana shi ta wurin aiko da mala'ikansa zuwa
ga bawansa Yohanna, 2 wanda ya shaida dukan abin da ya gani, wato, maganar
Allah da kuma shaidar Yesu Kiristi. 3 Mai albarka ne wanda yake karanta waɗannan
kalmomin annabci, masu albarka ne kuma waɗanda suke jinsu, suke kuma sa abin
da aka rubuta a ciki a zuciya, domin lokaci ya yi kusa.

*Gaisuwa da yabo*

4 Daga Yohanna,

Zuwa ga ikkilisiyoyi bakwai da suke a lardin Asiya.

Alheri da salama gare ku daga shi wanda yake a yanzu, wanda yake a dā, da kuma
wanda zai zo, da kuma daga ruhohi bakwai da suke a gaban kursiyinsa, 5 da kuma
daga Yesu Kiristi, wanda yake amintaccen shaida, ɗan farin daga tashin matattu, da
kuma mai mulkin sarakunan duniya.

Gare shi wanda yake ƙaunarmu wanda kuma ya 'yantar da mu daga zunubanmu
ta wurin jininsa, 6 ya kuma mai da mu masarauta da firistoci don mu yi wa Allahnsa
da Ubansa hidima, a gare shi ɗaukaka da iko sun tabbata har abada abadin! Amin.
7 "Duba, yana zuwa cikin gizagizai,
kowane ido kuwa zai gan shi,
har da waɗanda suka soke shi";
dukan mutanen duniya kuwa "za su yi makoki dominsa."
Bari yǎ zama haka nan! Amin.
8 "Ni ne Alfa da kuma Omega," in ji Ubangiji Allah, "wanda yake a yanzu, wanda
yake a dā, da kuma wanda zai zo, Maɗaukaki."

*Wani kama da Ɗan Mutum*

9 Ni, Yohanna, ɗan'uwanku da kuma abokin tarayyarku cikin wahala da mulki,
da kuma haƙurin jimrewa da suke namu cikin Yesu, ina can tsibirin Fatmos saboda
maganar Allah da kuma saboda shaidar Yesu. 10 A Ranar Ubangiji ina cikin Ruhu,
sai na ji a bayana wata babbar murya kamar ƙaho, 11 wadda ta ce, "Rubuta a cikin
naɗaɗɗen littafi abin da ka gani ka kuma aika ta zuwa ga ikkilisiyoyi bakwai, zuwa
Afisa, Simirna, Fergamum, Tiyatira, Sardis, Filadelfiya, da kuma Lawodiseya."
12 Sai na juya don in ga muryar da take magana da ni. Da na juya kuwa sai na
ga alkukan fitilu bakwai na zinariya. 13 A tsakiyar alkukan kuwa akwai wani "kama
da ɗan mutum,"* saye da rigar da ya kai har ƙafafunsa da kuma ɗamarar zinariya
daure a ƙirjinsa. 14 Kansa da kuma gashin fari ne fat kamar ulu, fari kamar dusar
ƙanƙara, idanunsa kuwa kamar harshen wuta. 15 Sawunsa sun yi kamar tagullar da
take haske cikin matoya, muryarsa kuma ta yi kamar muryar ruwaye masu gudu.

* **1:13** Dubi Dan 7.13.

16 A hannunsa na dama ya riƙe taurari bakwai, daga bakinsa kuwa takobi mai kaifi
biyu ya fito. Fuskarsa ta yi kamar rana mai haskakawa da dukan haskenta.
17 Sa'ad da na gan shi, sai na fāɗi a gabansa sai ka ce matacce. Sai ya ɗibiya
hannunsa na dama a kaina ya ce, "Kada ka ji tsoro. Ni ne Farko da kuma Karshe.
18 Ni ne Rayayye, dā na mutu, ga shi kuwa ina a raye har abada abadin! Ina kuma
riƙe da mabuɗan mutuwa da na Hades.
19 "Saboda haka, ka rubuta abin da ka gani, abin da yake yanzu, da abin da zai
faru nan gaba. 20 Asirin taurari bakwai da ka gani a hannuna na dama da kuma
na alkukan fitilu bakwai na zinariya shi ne, Taurarin bakwai ɗin nan, mala'ikun
ikkilisiyoyi bakwai ne; alkukan fitilu bakwai ɗin nan kuma ikkilisiyoyi bakwai ne.

# 2

*Zuwa ga ikkilisiya a Afisa*

1 "Zuwa ga mala'ikan ikkilisiya a Afisa, ka rubuta,

Waɗannan su ne kalmomi na wannan wanda yake riƙe da taurari bakwai a hannunsa na dama yana kuma tafiya a tsakanin alkukan fitilu bakwai na zinariya.

2 Na san ayyukanka, faman aikinka da daurewarka. Na san cewa ba ka iya haƙuri
da mugayen mutane, ka gwada waɗanda suke cewa su manzanni ne, alhali kuwa
ba haka ba ne, ka kuwa tarar cewa su na ƙarya ne. 3 Kai kam ka daure ka kuma
jimre da wahala saboda sunana, ba ka kuwa gaji ba.
4 Duk da haka ina riƙe da wannan game da kai. Ka watsar da ƙaunarka ta farko.
5 Ka tuna da matsayinka a dā kafin ka fāɗi! Ka tuba ka kuma yi ayyukan da ka yi
da fari. In ba ka tuba ba, zan zo wajenka in ɗauke wurin ajiye fitilanka daga inda
yake. 6 Sai dai kana da wannan abu mai kyau. Ka ƙi ayyukan Nikolaitawa da ni
ma nake ƙi.
7 Duk mai kunnen ji, yǎ ji abin da Ruhu yake faɗa wa ikkilisiyoyi. Duk wanda ya ci nasara, zan ba shi ikon ci daga itacen rai, da yake cikin aljannar Allah.

*Zuwa ga ikkilisiya a Simirna*

8 "Zuwa ga mala'ikan ikkilisiya a Simirna, ka rubuta,

Waɗannan su ne kalmomin wannan da yake na Farko da na Karshe, wanda ya mutu ya kuma sāke tashi da rai.

9 Na san wahalarka da kuma talaucinka, duk da haka kai mai arziki ne! Na san
ɓata suna da waɗannan suke yi maka waɗannan da suke cewa su Yahudawa ne
alhali kuwa ba haka ba ne, su dai majami'ar Shaiɗan ne. 10 Kada ka ji tsoron
wahalar da kake gab da sha. Ina gaya maka, Iblis zai sa waɗansunku a kurkuku don yǎ gwada ku. Za ku sha tsanani na kwana goma. Ka yi aminci ko da za a kashe ka, ni kuwa zan ba ka rawanin rai.
11 Duk mai kunnen ji, yǎ ji abin da Ruhu yake faɗa wa ikkilisiyoyi. Duk wanda ya ci nasara mutuwa ta biyu ba za tǎ cuce shi ba ko kaɗan.

*Zuwa ga ikkilisiya a Fergamum*

12 "Zuwa ga mala'ikan ikkilisiya a Fergamum, ka rubuta,

Waɗannan su ne kalmomin wannan wanda yake da takobi mai kaifi biyu.

13 Na san inda kake da zama, inda Shaiɗan yana da gadon sarautarsa. Duk da
haka ka riƙe sunana da gaske. Ba ka yi mūsun bangaskiyarka gare ni ba, har ma
a kwanakin Antifas, amintaccen mashaidina, wanda aka kashe a birninku, inda
Shaiɗan yake zama.
14 Duk da haka, ina da abubuwa kima game da kai. Kana da mutane a can
waɗanda suke riƙe da koyarwar Bala'am, wanda ya koya wa Balak yǎ ja hankalin
Isra'ilawa su yi zunubi ta wurin cin abincin da aka miƙa wa gumaka hadaya,
su kuma yi fasikanci. 15 Haka ma kana da waɗanda suke riƙe da koyarwar
Nikolaitawa. 16 Saboda haka ka tuba! In ba haka ba, zan zo wajenka ba da daɗewa
ba in yaƙe su da takobin bakina.
17 Duk mai kunnen ji, yǎ ji abin da Ruhu yake faɗa wa ikkilisiyoyi. Duk wanda
ya ci nasara zan ba shi kaɗan daga cikin ɓoyayyiyar Manna. Zan kuma ba shi farin
dutse tare da sabon suna a rubuce a bisansa, sananne kawai ga mai karɓan dutsen.

*Zuwa ga ikkilisiya a Tiyatira*

18 "Zuwa ga mala'ikan ikkilisiya a Tiyatira, ka rubuta,

Waɗannan su ne kalmomin Ɗan Allah, wanda idanunsa suna kama da harshen
wuta wanda kuma ƙafafunsa suna kama da tagullar da aka goge.

19 Na san ayyukanka, ƙaunarka da bangaskiyarka, hidimarka da daurewarka,
kuma cewa kana yin abubuwa a yanzu fiye da abin da ka yi da farko.
20 Duk da haka, ina da wannan game da kai. Kana haƙuri da matan nan Yezebel,
wadda take kira kanta annabiya. Ta wurin koyarwarta tana ɓad da bayina ga yin
fasikanci suka kuma ci abincin da aka miƙa wa gumaka. 21 Na ba ta lokaci tǎ
tuba daga fasikancinta, amma ba ta da niyya. 22 Don haka zan jefa ta a kan gadon
wahala, zan kuma sa waɗanda suke zina da ita, su sha azaba ƙwarai, sai dai in
sun tuba daga hanyoyinta. 23 Zan kashe 'ya'yanta. Sa'an nan dukan ikkilisiyoyi za
su san cewa ni ne mai bincika zukata da tunani, zan kuwa sāka wa kowannenku
gwargwadon ayyukansa.
24 Yanzu, ina ce wa sauranku da kuke a Tiyatira, ku da ba ku riƙe da koyarwarta
ba kuma ba ku koyi abin da suke kira zurfafan asiran Shaiɗan, 'Ba zan ƙara muku
wani nauyi ba. 25 Sai dai ku riƙe abin da kuke da shi har sai na zo.'
26 Gare shi wanda ya ci nasara ya kuma aikata nufina har ƙarshe, zan ba shi iko
a kan al'ummai. 27 'Zai yi mulki a kansu da sandar sarauta ta ƙarfe, zai farfashe
su, kamar tukwanen yumɓu'*kamar yadda na karɓi iko daga Ubana. 28 Zan kuma
ba shi tauraron asubahi. 29 Duk mai kunnen ji, yǎ ji abin da Ruhu yake faɗa wa
ikkilisiyoyi.

# 3

*Zuwa ga ikkilisiya a Sardis*

1 "Zuwa ga mala'ikan ikkilisiya a Sardis, ka rubuta,

Waɗannan su ne kalmomi, na wanda yake riƙe da ruhohi bakwai na Allah da
kuma taurari bakwai.

Na san ayyukanka; ana ganinka kamar rayayye, amma kai matacce ne. 2 Ka
farka! Ka ƙarfafa abin da ya rage wanda kuma yake bakin mutuwa, don ban ga
ayyukanka cikakke ne ba a gaban Allahna. 3 Saboda haka, ka tuna fa, abin da ka

* **2:27** Zab 2.9

karɓa ka kuma ji; ka yi biyayya da shi, ka kuma tuba. Amma in ba ka farka ba,
zan zo kamar ɓarawo, ba kuwa za ka san lokacin da zan zo maka ba.
4 Duk da haka kana da mutane kima cikin Sardis waɗanda ba su ɓata tufafinsu
ba. Za su yi tafiya tare da ni, saye da fararen tufafi, don sun cancanta. 5 Wanda
ya ci nasara, kamar su, za a sanya masa fararen tufafi. Ba zan taɓa share sunansa
daga cikin littafin rai ba, sai dai zan shaida sunansa a gaban Ubana da mala'ikunsa.
6 Duk mai kunnen ji, yă ji abin da Ruhu yake faɗa wa ikkilisiyoyi.

### *Zuwa ga ikkilisiya a Filadelfiya*

7 "Zuwa ga mala'ikan ikkilisiya a Filadelfiya, ka rubuta,

Waɗannan su ne kalmomi, na wanda yake mai tsarki da kuma gaskiya, wanda
yake riƙe da mabuɗin Dawuda. Abin da ya buɗe ba mai rufewa, abin da kuma ya
rufe ba mai buɗewa.

8 Na san ayyukanka. Duba, na sa a gabanka buɗaɗɗen ƙofa wadda ba mai iya
rufewa. Na san cewa kana da ɗan ƙarfi, duk da haka ka kiyaye maganata ba ka
kuwa yi mūsun sunana ba. 9 Zan sa waɗanda suke na majami'ar Shaiɗan, waɗanda
suke cewa su Yahudawa ne alhali kuwa ba haka ba ne, sai dai maƙaryata, zan sa
su zo su fāɗi a ƙasa a gabanka su kuma shaida cewa na ƙaunace ka. 10 Da yake ka
kiyaye umarnina ta wurin jimrewa, ni ma zan tsare ka daga lokacin nan na gwaji
wanda zai zo bisan dukan duniya don a gwada waɗanda suke zama a duniya.
11 Ina zuwa ba da daɗewa ba. Ka riƙe abin da kake da shi, don kada wani ya
karɓe rawaninka. 12 Duk wanda ya ci nasara zan mai da shi ginshiƙi a haikalin
Allahna. Ba kuwa zai sāke barin wurin ba. Zan rubuta a kansa sunan Allahna da
kuma sunan birnin Allahna, sabuwar Urushalima, wadda take saukowa daga sama
daga Allahna; ni kuma zan rubuta a kansa sabon sunana. 13 Duk mai kunnen ji, yă
ji abin da Ruhu yake faɗa wa ikkilisiyoyi.

### *Zuwa ga ikkilisiya a Lawodiseya*

14 "Zuwa ga mala'ikan ikkilisiya a Lawodiseya, ka rubuta,

Waɗannan su ne kalmomina Amin, amintaccen mashaidi mai gaskiya, da kuma
mai mulkin halittar Allah.

15 Na san ayyukanka, ba ka da sanyi ba ka kuma da zafi. Na so da kai ɗaya ne
daga ciki, ko sanyi, ko zafi! 16 Amma domin kana tsaka-tsaka ba zafi ba, ba kuma
sanyi ba, ina dab da tofar da kai daga bakina. 17 Ka ce, 'Ina da arziki; na sami
dukiya ba na kuma bukatar kome.' Amma ba ka gane ba cewa kai matsiyaci ne,
abin tausayi, matalauci, makaho kana kuma tsirara. 18 Na shawarce ka ka sayi
zinariyar da aka tace cikin wuta daga gare ni, don ka yi arziki; da fararen tufafi ka
sa, don ka rufe kunyar tsirancinka; da kuma maganin ido ka sa a idanunka, don
ka gani.
19 Waɗanda nake ƙauna su nake tsawata wa, nake kuma horo. Saboda haka ka
yi himma ka tuba. 20 Ga ni! Ina tsaye a bakin ƙofa, ina ƙwanƙwasawa. Duk wanda
ya ji muryata ya kuma buɗe ƙofar, zan shiga in kuma ci tare da shi, shi kuma tare
da ni.
21 Duk wanda ya ci nasara, zan ba shi ikon zama tare da ni a kursiyina, kamar
yadda na ci nasara, kuma ina zaune tare da Ubana a kursiyinsa. 22 Duk mai kunnen
ji, yă ji abin da Ruhu yake faɗa wa ikkilisiyoyi."

# 4

*Kursiyi a sama*

1 Bayan wannan sai na duba, a can kuma a gabana ga ƙofa a buɗe a sama. Sai
muryar da na ji da fari da take magana da ni mai kama da busar ƙaho ta ce, “Hauro
nan, zan kuma nuna maka abin da lalle zai faru bayan wannan.” 2 Nan da nan
sai ga ni cikin Ruhu, a can a gabana kuwa ga kursiyi a cikin sama da wani zaune a
kansa. 3 Wannan mai zama a can kuwa yana da kamannin dutsen yasfa da karneliya.
Bakan gizo, mai kama da zumurrudu, ya kewaye kursiyin. 4 Kewaye da kursiyin kuwa
akwai waɗansu kursiyoyi ashirin da huɗu, zaune a kansu kuwa dattawa ashirin da
huɗu ne. Suna saye da fararen tufafi suna kuma da rawanin zinariya a kawunansu.
5 Daga kursiyin hasken walƙiya yana ta fitowa, da ƙararraki da kuma tsawa. A gaban
kursiyin, fitilu bakwai suna ci. Waɗannan ne ruhohi bakwai na Allah. 6 Haka kuma
a gaban kursiyin akwai wani abu mai kama da tekun gilashi, yana ƙyalli kamar
madubi.

A tsakiya kuwa, kewaye da kursiyin, akwai halittu huɗu masu rai, cike kuma suna
da idanu gaba da baya. 7 Halitta ta fari tana kama da zaki, ta biyun kuwa tana kama
da bijimi, ta ukun kuma tana da fuska kamar ta mutum, ta huɗun kuma tana kama
da gaggafa mai tashi sama. 8 Kowace a cikin halittu huɗu masu rai ɗin nan tana da
fikafikai guda shida, tana kuma cike da idanu a ko'ina, har ma ƙarƙashin fikafikanta.
Dare da rana ba sa fasa cewa,

“ ‘Mai Tsarki, Mai Tsarki, Mai Tsarki
shi ne Ubangiji Allah Maɗaukaki,’
wanda yake a dā, wanda yake a yanzu, wanda kuma yake nan gaba.”

9 Duk lokacin da halittu masu ran nan suka rera ɗaukaka, girma da kuma godiya ga
wannan wanda yake zaune a kan kursiyin da kuma wanda yake mai rai har abada
abadin, 10 sai dattawa ashirin da huɗun nan su fāɗi a ƙasa a gaban wannan wanda
yake zaune a kursiyin, su yi sujada wa wannan wanda yake da rai har abada abadin.
Sukan ajiye rawaninsu a gaban kursiyin suna cewa,

11 “Ya Ubangijinmu da Allahnmu,
ka cancanci ɗaukaka da girma da iko,
domin ka halicci dukan abubuwa,
kuma ta wurin nufinka aka halicce su
suka kuma kasance.”

# 5

*Naɗaɗɗen littafi da kuma Ɗan Ragon*

1 Sa'an nan na ga a hannun damar wannan wanda yake zaune a kursiyin naɗaɗɗen
littafi da rubutu a ciki da wajensa an kuma hatimce shi da hatimai bakwai. 2 Na kuma
ga wani babban mala'ika yana shela da babbar murya cewa, “Wa ya cancanta yǎ ɓalle
hatiman nan yǎ kuma buɗe naɗaɗɗen littafin?” 3 Amma ba wani a sama ko a ƙasa
ko a ƙarƙashin ƙasan da ya iya buɗe naɗaɗɗen littafin ko ma yǎ duba cikinsa. 4 Na
yi ta kuka domin ba a iya samun wanda ya cancanta yǎ buɗe naɗaɗɗen littafin ko yǎ
duba cikinsa ba. 5 Sai ɗaya daga cikin dattawan ya ce mini, “Kada ka yi kuka! Duba,
Zakin kabilar Yahuda, da kuma Tushen Dawuda ya ci nasara. Ya iya buɗe naɗaɗɗen
littafin da hatimansa bakwai.”

6 Sa'an nan na ga Ɗan Rago, yana kamar an yanka, tsaye a tsakiyar kursiyin, halittu
huɗun nan masu rai da kuma dattawan an sun kewaye shi. Yana da ƙahoni bakwai
da idanu bakwai, waɗanda suke ruhohi bakwai na Allah da aka aika cikin dukan
duniya. 7 Ya zo ya karɓi naɗaɗɗen littafin daga hannun dama na wannan wanda
yake zaune a kursiyin. 8 Bayan ya karɓa, sai halittu huɗun nan masu rai da kuma

dattawan nan ashirin da huɗu suka fāɗi ƙasa a gaban Ɗan Ragon. Kowannensu yana da garaya kuma suna riƙe da kaskon zinariya cike da turare, waɗanda suke addu'o'in tsarkaka.
9 Suka rera sabuwar waƙa,
"Ka cancanci ka karɓi naɗaɗɗen littafin
ka kuma buɗe hatimansa,
domin an kashe ka,
da jininka kuma ka sayi mutane wa Allah,
daga kowace kabila da harshe da mutane da kuma al'umma.
10 Ka mai da su masarauta da kuma firistoci, don su yi wa Allahnmu hidima,
kuma za su yi mulki a duniya."
11 Sai na duba na kuma ji muryar mala'iku masu yawa, yawansu kuwa ya kai dubu
dubbai, da kuma dubu goma sau dubu goma. Suka kewaye kursiyin da halittu huɗun
nan masu rai da kuma dattawan nan. 12 Da babbar murya suka rera,
"Macancanci ne Ɗan Ragon nan da aka kashe,
don yǎ sami iko da wadata da hikima da ƙarfi
da girma da ɗaukaka da kuma yabo!"
13 Sa'an nan na ji kowace halitta a sama da ƙasa da ƙarƙashin ƙasa da kuma bisan
teku, da kome da yake cikinsu yana rerawa,
"Gare shi mai zama a kan kursiyin da kuma ga Ɗan Ragon
yabo da girma da ɗaukaka da iko,
sun tabbata har abada abadin!"
14 Sai halittu huɗun nan masu rai suka ce, "Amin", dattawan kuma suka fāɗi suka yi
sujada.

# 6

*Hatimai*

1 Na kalli yayinda Ɗan Ragon ya buɗe hatimin farko na hatimai bakwai ɗin nan.
Sai na ji ɗaya daga cikin halittu huɗun nan masu rai ya yi magana da murya mai
kama da tsawa ya ce, "Zo!" 2 Na duba, can kuwa a gabana ga wani farin doki! Mai
hawansa yana riƙe da baka, aka kuma ba shi rawani, ya yi sukuwa ya fito kamar mai
nasara da ya kutsa don nasara.
3 Sa'ad da Ɗan Ragon ya buɗe hatimi na biyun, sai na ji halitta mai rai na biyu ya
ce, "Zo!" 4 Sai wani doki ya fito, ja wur. Aka ba wa mai hawansa iko yǎ ɗauke salama
daga duniya yǎ kuma sa mutane su kashe juna. Aka ba shi babban takobi.
5 Sa'ad da Ɗan Ragon ya buɗe hatimi na uku, sai na ji halitta mai rai na uku ya
ce, "Zo!" Na duba, can a gabana kuwa ga wani baƙin doki! Mai hawansa yana riƙe
da abubuwan awo guda biyu a hannunsa. 6 Sai na ji wani abu mai ƙara kamar
wata murya a tsakiyar halittu huɗun nan masu rai tana cewa, "Kwatan alkama don
albashin aikin yini, da kuma kwata uku na sha'ir don albashin yini guda, kada kuwa
ka ɓata man da ruwan inabi!"
7 Sa'ad da Ɗan Ragon ya buɗe hatimi na huɗu, sai na ji muryar halitta mai rai na
huɗu ya ce, "Zo!" 8 Na duba, can a gabana kuwa ga ƙodaɗɗen doki! An ba wa mai
hawansa suna Mutuwa, Hades kuwa yana biye da shi. Aka ba su iko a kan kashi
ɗaya bisa huɗu na duniya don su yi kisa da takobi, yunwa da annoba, har ma da
namomin jeji na duniya.
9 Sa'ad da ya buɗe hatimi na biyar, sai na ga a ƙarƙashin bagaden rayukan
waɗanda aka kashe saboda maganar Allah da kuma shaidar da suka yi. 10 Suka yi
kira da babbar murya suka ce, "Ya Ubangiji Mai Iko Duka, Mai Tsarki da kuma Mai
Gaskiya, sai yaushe za ka shari'anta mazaunan duniya ka kuma ɗauki mana fansar
jininmu?" 11 Sai aka ba wa kowannensu farin riga, aka kuma faɗa musu su ɗan jira

kaɗan sai an cika adadin abokansu masu hidima da kuma 'yan'uwansu waɗanda za
a kashe kamar yadda su ma aka kashe su.
[12] Ina kallo yayinda ya buɗe hatimi na shida. Sai aka yi babban girgizar ƙasa.
Rana ta zama baƙa kamar gwado na gashin akuya, wata kuma gaba ɗaya ya zama ja
wur kamar jini, [13] taurarin sararin sama suka fāɗɗāɗi a ƙasa, kamar yadda ɗanyun
'ya'yan ɓaure suke fāɗuwa daga itacen ɓaure sa'ad da iska mai ƙarfi ta jijjiga shi.
[14] Sararin sama kuwa ya janye kamar naɗaɗɗen littafi, ya yi ta naɗewa, aka kuma
kawar da kowane dutse da kowane tsibiri daga wurinsa.
[15] Sa'an nan sarakunan duniya, hakimai, jarumawa, masu arziki, masu ƙarfi, da
kowane bawa da kuma kowane 'yantacce ya ɓoye a cikin koguna da kuma cikin
duwatsun tsaunuka. [16] Suka kira duwatsu da tsaunuka suna cewa, "Ku fāɗi a kanmu
ku kuma ɓoye mu daga fuskar wannan mai zama a kan kursiyi da kuma daga fushin
Ɗan Ragon nan! [17] Gama babbar ranar fushinsu ta zo, wa kuwa zai iya tsayawa?"

# 7

*An yi wa 144,000 hatimi*

[1] Bayan wannan, na ga mala'iku huɗu, a tsaye a kusurwoyi huɗu na duniya, suna
tsare iskoki huɗu na duniya, domin su hana wani iska hurawa a bisan ƙasa ko a
bisan teku ko a bisa wani itace. [2] Sai na ga wani mala'ika yana zuwa daga gabas,
yana da hatimin Allah mai rai. Ya yi kira da babbar murya wa mala'ikun nan huɗu
da aka ba su iko su cuci ƙasa da teku ya ce, [3] "Kada ku cuci ƙasa ko teku ko kuma
itatuwa sai bayan mun sa hatimi a goshin dukan bayin Allahnmu." [4] Sai na ji yawan
waɗanda aka sa musu hatimi. Su 144,000 daga dukan kabilan Isra'ila.

[5] Daga kabilar Yahuda mutum 12,000 ne aka sa musu hatimin,
daga kabilar Ruben mutum 12,000,
daga kabilar Gad mutum 12,000,
[6] daga kabilar Asher mutum 12,000,
daga kabilar Naftali mutum 12,000,
daga kabilar Manasse mutum 12,000,
[7] daga kabilar Simeyon mutum 12,000,
daga kabilar Lawi mutum 12,000,
daga kabilar Issakar mutum 12,000,
[8] daga kabilar Zebulun mutum 12,000,
daga kabilar Yusuf mutum 12,000,
daga kabilar Benyamin mutum 12,000.

*Babban taro sanye da fararen tufafi*

[9] Bayan wannan sai na duba, can a gabana kuwa ga wani taro mai girma, wanda
ba mai iya ƙirgawa, daga kowace al'umma, kabila, mutane da kuma harshe, suna
tsaye a gaban kursiyin da kuma gaban Ɗan Ragon nan. Suna saye da fararen tufafi
suna kuma riƙe da rassan dabino a hannuwansu. [10] Suka tā da murya da ƙarfi suna
cewa,
"Ceto na Allahnmu ne,
wanda yake zaune a bisan kursiyi,
da kuma na Ɗan Ragon."
[11] Dukan mala'iku suna tsaye kewaye da kursiyin da kuma kewaye da dattawan tare
da halittu huɗun nan masu rai. Suka fāɗi da fuskokinsu ƙasa a gaban kursiyin suka
kuma yi wa Allah sujada, [12] suna cewa,
"Amin!
Yabo da ɗaukaka,

da hikima da godiya da girma
da iko da ƙarfi
sun tabbata ga Allahnmu har abada abadin.
Amin!”
13 Sai ɗaya daga cikin dattawan ya tambaye ni ya ce, “Waɗannan da suke saye da
fararen tufafi su wane ne, daga ina kuma suka fito?”
14 Na amsa na ce, “Ranka yă daɗe, kai ka sani.”
Sai ya ce, “Waɗannan su ne waɗanda suka fito daga matsananciyar wahala; sun
wanke tufafinsu suka kuma mai da su farare da jinin Ɗan Ragon nan. 15 Saboda haka,
“suna a gaban kursiyin Allah
suna masa hidima dare da rana a cikin haikalinsa;
kuma wannan mai zaune a kursiyin zai shimfiɗa tentinsa a bisansu.
16 ‘Ba za su sāke jin yunwa ba;
ba za su kuma sāke jin ƙishirwa ba.
Rana ba za tă buga su ba,’
ko kuma kowane irin zafin ƙuna.
17 Gama Ɗan Ragon da yake a tsakiyar kursiyin zai zama makiyayinsu;
‘zai bi da su zuwa ga maɓulɓular ruwan rai.’
‘Allah kuwa zai share dukan hawaye daga idanunsu.’ ”

# 8

### *Hatimi na bakwai da kaskon zinariya*

1 Sa’ad da ya buɗe hatimi na bakwai, sai aka yi shiru a sama na kusan rabin sa’a.
2 Sai na ga mala’iku bakwai da suke tsayawa a gaban Allah, a gare su kuwa aka ba
da ƙahoni bakwai.
3 Wani mala’ika, da yake da kaskon zinariyar da ake zuba turare, ya zo ya tsaya kusa
da bagaden. Aka ba shi turare da yawa don yă miƙa tare da addu’o’in dukan tsarkaka
a bisa bagaden zinariya a gaban kursiyin. 4 Hayaƙin turaren tare da addu’o’in
tsarkaka, suka hau zuwa gaban Allah daga hannun mala’ikan. 5 Sai mala’ikan ya
ɗauki kaskon, ya cika shi da wuta daga bagaden, ya kuma wurga shi bisan duniya;
sai aka yi ta yin tsawa, ƙararraki, walƙiya, da kuma girgizar ƙasa.

### *Kahoni*

6 Sai mala’iku bakwai ɗin nan da suke da ƙahoni bakwai suka shirya don su busa
su.
7 Mala’ika na fari ya busa ƙahonsa, sai ga ƙanƙara da wuta haɗe da jini, aka kuma
wurga su bisan duniya. Kashi ɗaya bisa uku na duniya ya ƙone, kashi ɗaya bisa uku
na itatuwa suka ƙone, dukan ɗanyar ciyawa kuma ta ƙone.
8 Mala’ika na biyu ya busa ƙahonsa, sai ga wani abu kamar babban dutse mai cin
wuta, aka jefa cikin teku. Kashi ɗaya bisa uku na teku ya zama jini, 9 kashi ɗaya bisa
uku na halittu masu rai da suke cikin tekun suka mutu, kashi ɗaya bisa uku kuma
na jiragen ruwa kuma suka hallaka.
10 Mala’ika na uku ya busa ƙahonsa, sai wani babban tauraro mai cin wuta kamar
toci, ya fāɗi daga sararin sama, a kan kashi ɗaya bisa uku na koguna da kuma a bisa
maɓulɓulan ruwa 11 sunan tauraron kuwa Maɗaci. Kashi ɗaya bisa uku na ruwaye ya
zama mai ɗaci, mutane da yawa kuma suka mutu saboda shan ruwan, don ɗacinsa.
12 Mala’ika na huɗu ya busa ƙahonsa, sai aka bugi kashi ɗaya bisa uku na rana,
kashi ɗaya bisa uku na wata, da kashi ɗaya bisa uku na taurari, har kashi ɗaya bisa
uku nasu ya duhunta. Kashi ɗaya bisa uku na yini ya kasance babu haske, haka ma
kashi ɗaya bisan uku na dare.

[13] Yayinda nake kallo, sai na ji gaggafar da take tashi sama a tsakiyar sararin sama ta yi kira da babbar murya ta ce, "Kaito! Kaito! Kaiton mazaunan duniya, in an yi busan sauran ƙahonin da mala'ikun nan uku suke shirin busawa!"

# 9

[1] Mala'ika na biyar ya busa ƙahonsa, sai na ga tauraron da ya fāɗo duniya daga
sararin sama. Aka ba wa tauraron mabuɗin ramin Abis. [2] Da ya buɗe Abis ɗin, sai
hayaƙi ya taso daga cikin kamar hayaƙin matoya mai girma. Hayaƙin nan daga Abis
ya duhunta rana da sararin sama. [3] Daga cikin hayaƙin kuwa fāri suka fito zuwa
cikin duniya aka kuma ba su iko irin na kunaman duniya. [4] Aka faɗa musu kada su
yi wa ciyawa na duniya lahani ko wani tsiro ko itace, sai dai su yi wa mutanen da ba
su da hatimin Allah a goshinsu kaɗai lahani. [5] Ba a ba su iko su kashe su ba, sai dai
su ba su azaba na watanni biyar. Azabar da suka sha kuwa ya yi kamar ta harbin
kunama sa'ad da ta harbi mutum. [6] Cikin waɗannan kwanakin mutane za su nemi
mutuwa, amma ba za su samu ba; za su yi marmarin mutuwa, amma mutuwa za tă
ɓace musu.
[7] Kamannin fārin nan kuwa yana kama da dawakan da aka shirya don yaƙi. A
kawunansu kuwa da wani abu da ya yi kamar rawanin zinariya, fuskokinsu kuma sun
yi kamar fuskokin mutane. [8] Gashin kansu ya yi kamar gashin kan mata, haƙoransu
kuma sun yi kamar haƙoran zakoki. [9] Suna da sulkuna kamar sulkunan ƙarfe,
ƙarar fikafikansu kuma ta yi kamar motsin dawakai da kekunan yaƙi masu yawa
da suke rugawa zuwa yaƙi. [10] Suna da wutsiyoyi da ƙari kamar kunamai, kuma a
wutsiyoyinsu suna da iko su ba wa mutane azaba na wata biyar. [11] Suna da sarkin
da yake mulki a bisansu wanda yake mala'ikan Abis, wanda sunansa a harshen
Yahudawa shi ne Abaddon, da harshen Hellenawa kuwa shi ne, Afolliyon.*
[12] Bala'i na fari ya wuce, sauran bala'i biyu suna nan zuwa.
[13] Mala'ika na shida ya busa ƙahonsa, sai na ji murya tana fitowa daga ƙahonin
bagaden zinariya da suke a gaban Allah. [14] Ta ce wa mala'ika na shida da yake da
ƙahon, "Ka saki mala'iku huɗun nan da suke a daure a babban kogin Yuferites."
[15] Mala'iku huɗun nan kuwa da aka shirya musamman don wannan sa'a da kuma
don wannan rana da wata da kuma shekara aka sake su domin su kashe kashi ɗaya
bisa uku na 'yan Adam. [16] Yawan rundunan masu hawan dawakan nan mutum
miliyon ɗari biyu ne. Na ji adadinsu.
[17] Dawakai da masu hawansu da na gani cikin wahayina sun yi kamar. Sulkunansu
ja wur ne, baƙin shuɗi, da kuma rawaya kamar farar wuta. Kawunan dawakan sun
yi kamar kawunan zakoki, daga bakunansu kuwa wuta, hayaƙi, da farar wuta suna
fitowa. [18] Aka kashe kashi ɗaya bisa uku na 'yan Adam da annobai uku na wuta,
hayaƙi da farar wuta da suka fito daga bakunansu. [19] Karfin dawakan nan kuwa
yana a bakunansu da wutsiyoyinsu; gama wutsiyoyinsu suna kama da macizai masu
kawuna, da wutsiyoyin ne kuma suke yi wa mutane rauni.
[20] Sauran 'yan Adam da ba a kashe ta wajen waɗannan annobai ba kuwa har wa
yau ba su tuba daga aikin hannuwansu ba; ba su daina bauta wa aljanu, da gumakan
zinariya, azurfa, tagulla, dutse da na itace, gumakan da ba sa iya gani ko ji ko tafiya
ba. [21] Ba su kuma tuba daga kisankansu, sihirinsu, fasikancinsu ko kuma daga sace-
sacensu ba.

# 10

### *Mala'ika da ƙaramin naɗaɗɗen littafi*

* **9:11** Abaddon da kuma Afolliyon suna nufin Maihallakarwa.

1 Sai na ga wani babban mala'ika yana saukowa daga sama. An lulluɓe shi da
girgije, bakan gizo kuma yana kansa; fuskarsa tana kama da rana, ƙafafunsa kuma
suna kama da ginshiƙan wuta. 2 Yana riƙe da ɗan ƙaramin naɗaɗɗen littafi, wanda
yake a buɗe a hannunsa. Ya kafa ƙafarsa ta dama a kan teku ƙafarsa ta hagu kuma
a kan ƙasa, 3 ya kuma yi ihu da ƙarfi kamar rurin zaki. Da ya yi ihun, sai muryoyin
tsawan nan bakwai suka yi magana. 4 Sa'ad da tsawan nan bakwai kuwa suka yi
magana, ina dab da rubutawa; amma na ji wata murya daga sama ta ce, "Rufe abin
da tsawan nan bakwai suka faɗa kada ka rubuta."
5 Sai mala'ikan da na gani na tsaye a teku da ƙasa ya ɗaga hannunsa na dama
sama. 6 Ya kuma yi rantsuwa da wannan wanda yake raye har abada abadin, wanda
ya halicci sammai da dukan abin da yake cikinsu, duniya da dukan abin da yake
cikinta, da kuma teku da dukan abin da yake cikinsa, ya kuma ce, "Babu sauran
jinkiri! 7 Amma a ranakun da mala'ika na bakwai na dab da busa ƙahonsa, za a cika
asirin Allah, kamar yadda ya sanar wa bayinsa annabawa."
8 Sai muryar da na ji daga sama ta sāke magana da ni ta ce, "Tafi, ka karɓi
naɗaɗɗen littafin da yake a buɗe a hannun mala'ikan da yake tsaye bisa teku da
ƙasa."
9 Sai na je wajen mala'ikan na ce masa yă ba ni ƙaramin naɗaɗɗen littafin. Ya ce
mini, "Karɓa ka ci. Zai sa cikinka yă yi tsami, amma 'a bakinka zai zama da zaƙi
kamar zuma.' " 10 Na karɓi ƙaramin naɗaɗɗen littafin daga hannun mala'ikan na
kuma ci. Ya yi zaƙi kamar zuma a bakina, amma sa'ad da na cinye, cikina ya yi
tsami. 11 Sa'an nan aka ce mini, "Dole ne ka sāke yin annabci game da mutane masu
yawa, al'ummai, harsuna da kuma sarakuna."

# 11

*Shaidu biyu*

1 Aka ba ni ƙara kamar sandan awo aka kuma ce mini, "Tafi ka auna haikalin
Allah da bagaden, ka kuma ƙirga waɗanda suke sujada a can. 2 Sai dai kada ka haɗa
da harabar waje; kada ka auna ta, domin an ba da ita ga Al'ummai. Za su tattaka
birni mai tsarki har watanni 42. 3 Zan kuma ba wa shaiduna nan biyu iko, za su
kuwa yi annabci na kwanaki 1,260, saye da gwadon makoki." 4 Waɗannan su ne
itatuwan zaitun biyu da kuma alkukai biyu da suke tsaye a gaban Ubangijin duniya.
5 Duk wanda ya yi ƙoƙari yin musu lahani, wuta za tă fito daga bakunansu ta cinye
abokan gābansu. Haka ne duk mai niyyar yin musu lahani zai mutu. 6 Waɗannan
mutane suna da iko su kulle sararin sama don kada a yi ruwan sama a lokacin da
suke annabci; suna kuma da iko su juye ruwaye su zama jini su kuma bugi duniya
da kowace irin annoba a duk lokacin da suke so.
7 To, da suka gama shaidarsu, dabbar da takan fito daga Abis za tă kai musu
hari, tă kuwa sha ƙarfinsu tă kuma kashe su. 8 Gawawwakinsu za su kasance a
kwance a titin babban birni, wanda a misalce ake kira Sodom da Masar, inda kuma
aka gicciye Ubangijinsu. 9 Kwana uku da rabi mutane daga kowace jama'a, kabila,
harshe da kuma al'umma za su yi ta kallon gawawwakinsu su kuma ƙi binne su.
10 Mazaunan duniya za su ƙyaface su kuma yi biki ta wurin aika kyautai wa juna,
domin waɗannan annabawan nan biyu ne suka azabtar da mazaunan duniya.
11 Amma bayan kwana uku da rabi ɗin numfashin rai daga Allah ya shige su, suka
kuwa tashi tsaye, tsoro kuma ya kama waɗanda suka gan su. 12 Sai suka ji wata
babbar murya daga sama tana ce musu, "Ku hauro nan." Suka kuwa haura zuwa
sama cikin girgije, yayinda abokan gābansu suna kallo.

13 A wannan sa'a aka yi wata babbar girgizar ƙasa kashi ɗaya bisa goma kuma na
birnin ya rushe. Aka kashe mutane dubu bakwai a girgizar ƙasar, waɗanda suka
tsira kuwa suka ji tsoro suka ɗaukaka Allah na sama.
14 Kaito na biyu ya wuce; kaito na uku yana zuwa ba da daɗewa ba.

*Kaho na bakwai*

15 Mala'ika na bakwai ya busa ƙahonsa, sai aka ji muryoyi masu ƙarfi a sama da
suka ce,
"Mulkin duniya ya zama
mulkin Ubangijinmu da na Kiristinsa,
zai kuwa yi mulki har abada abadin."
16 Sai dattawan nan ashirin da huɗu da suke zaune a kursiyoyinsu a gaban Allah,
suka fāɗi da fuskokinsu a ƙasa suka kuma yi wa Allah sujada, 17 suna cewa,
"Muna maka godiya ya Ubangiji Allah, Maɗaukaki,
wanda yake a yanzu, shi ne kuma a dā,
domin ka karɓi ikonka mai girma
ka kuma fara mulki.
18 Al'ummai suka yi fushi;
fushinka kuwa ya zo.
Lokaci ya yi don a shari'anta matattu,
da kuma don sākawa wa bayinka annabawa
da tsarkakanka da kuma su waɗanda suke girmama sunanka,
ƙarami da babba,
don kuma hallakar da waɗanda suka hallaka duniya."
19 Sa'an nan aka buɗe haikalin Allah da yake a sama, kuma a cikin haikalinsa aka
ga akwatin alkawarinsa. Sai kuwa ga walƙiya, ƙararraki, tsawa, girgizar ƙasa, da
kuma ƙanƙara masu girma.

# 12

*Mace da ƙaton maciji*

1 Babbar alama mai banmamaki ta bayyana a sama, mace tana lulluɓe da rana,
da kuma wata a ƙarƙashin sawunta, akwai kuma rawani mai taurari goma sha biyu
a kanta. 2 Tana da ciki ta kuma yi kuka mai zafi yayinda take gab da haihuwa.
3 Sai wata alama ta bayyana a sama, wani babban jan maciji mai kawuna bakwai da
ƙahoni goma da rawani bakwai a kan kawunansa. 4 Wutsiyarsa ta share kashi ɗaya
bisa uku na taurari daga sararin sama ta kuma zubar da su ƙasa. Katon jan macijin
ya tsaya a gaban macen wadda take gab da haihuwa, don yǎ cinye ɗanta nan take
bayan an haife shi. 5 Ta haifi ɗa, namiji, wanda zai yi mulkin dukan al'ummai da
sandar ƙarfe. Aka fyauce ɗanta zuwa wurin Allah da kuma kursiyinsa. 6 Sai macen
ta gudu zuwa hamada zuwa inda Allah ya shirya dominta, inda za a lura da ita har
kwana 1,260.
7 Aka kuwa yi yaƙi a sama. Mika'ilu da mala'ikunsa yaƙi macijin, maciji da
mala'ikunsa su ma suka mai da martani. 8 Amma macijin nan ba shi da isashen
ƙarfi, har suka rasa matsayinsu a sama. 9 Aka jefar da ƙaton jan macijin ƙasa, tsohon
maciji nan da ake kira Iblis, ko Shaiɗan, wanda ya ɓad da dukan duniya. Aka jefar
da shi ƙasa, tare da mala'ikunsa a duniya.
10 Sa'an nan na ji babbar murya daga sama tana cewa,
"Yanzu ceto da iko da mulkin Allahnmu,
da kuma ikon Kiristinsa.
Gama mai zargin 'yan'uwanmu,
wanda yake zarginsu a gaban Allahnmu dare da rana,

an jefar da shi ƙasa.
11 Sun ci nasara a kansa
ta wurin jinin Ɗan Ragon
da ta wurin kalmar shaidarsu;
ba su ƙaunaci rayukansu sosai
har da za su ja da baya daga mutuwa.
12 Saboda haka ku yi farin ciki, ku sammai,
da ku da kuke zaune a cikinsu!
Amma kaiton duniya da kuma teku,
gama Iblis ya sauko gare ku!
Ya cika da fushi,
domin ya san cewa lokacinsa ya rage kaɗan."
13 Sa'ad da macijin ya ga an jefar da shi a duniya, sai ya fafari macen nan da ta
haifi ɗa namiji. 14 Sai aka ba wa macen fikafikai biyu na babban gaggafa, don ta
tashi sama zuwa inda aka shirya mata a hamada, inda za a lura da ita na ɗan lokaci,
lokuta da rabin lokaci, inda macijin ba zai iya kaiwa ba. 15 Sa'an nan daga bakinsa
macijin ya kwarara ruwa kamar kogi, don ruwan ya cimma matan yǎ kuma kwashe
ta tare da ambaliya. 16 Amma ƙasa ta taimaki macen ta wurin buɗe bakinta ta kuma
shanye ruwan kogin da macijin ya kwarara daga bakinsa. 17 Sai macijin ya yi fushi da
macen ya kuma koma wajen sauran zuriyarta don yǎ yaƙe su waɗannan waɗanda
suke biyayya da umarnan Allah suke kuma riƙe da shaidar Yesu.

## 13

### *Dabbar daga teku*

1 Macijin kuwa* ya tsaya a bakin teku. Sai na ga wata dabba tana fitowa daga teku.
Tana da ƙahoni goma da kawuna bakwai, da kuma rawani goma a ƙahoninta, a
kowane kai kuwa akwai sunan saɓo. 2 Dabbar da na gani ta yi kamar damisa, amma
tana da ƙafafu kamar na beyar, bakinta kuma ya yi kamar na zaki. Macijin nan ya
ba wa dabbar ƙarfinsa da gadon sarautarsa da kuma ikonsa mai girma. 3 Ɗaya daga
cikin kawunan dabbar ya yi kamar yana da raunin da zai iya kashe shi, amma raunin
nan da zai iya kashe shi ya riga ya warke. Dukan duniya ta yi mamaki ta kuma bi
dabbar. 4 Mutane suka yi wa macijin sujada domin ya ba wa dabbar ikonsa, suka
yi wa dabbar sujada, suka kuma yi tambaya cewa, "Wane ne yake kama da dabban
nan? Wa zai iya yaƙe ta?"
5 Aka ba wa dabbar baki don ta faɗi kalmomin girman kai da na saɓo ta kuma yi
amfani da ikonta har watanni arba'in da biyu. 6 Ta buɗe bakinta don tǎ yi wa Allah
saɓo, ta kuma ɓata sunansa da kuma mazauninsa da na waɗanda suke zama a sama.
7 Aka ba ta iko tǎ yaƙi tsarkaka tǎ kuma ci nasara a kansu. Aka kuma ba ta iko bisa
kowace kabila, jama'a, harshe da kuma al'umma. 8 Dukan mazaunan duniya za su
yi wa dabbar sujada, dukan waɗanda ba a rubuta sunayensu a cikin littafin ran da
yake na Ɗan Ragon da aka yanka tun kafin halittar duniya ba.†
9 Duk mai kunne ji, bari yǎ ji.
10 Duk wanda aka ƙaddara ga bauta,
ga bauta zai tafi.
Duk wanda aka ƙaddara za a kashe da takobi,
da takobin za a kashe shi.
Wannan yana bukata haƙuri da aminci a gefen tsarkaka.

### *Dabba daga ƙasa*

---

* **13:1** Waɗansu rubuce-rubucen hannu na baya-bayan nan suna da Na kuma ne a nan

† **13:8** Ko kuwa rubutacce daga halittar duniya a littafin rai na Ɗan Ragon da aka yanka

11 Sai na ga wata dabba tana fitowa daga ƙasa. Tana da ƙahoni biyu kamar ɗan
rago, amma ta yi magana kamar maciji. 12 Ta mori dukan ikon dabban nan ta fari a
madadinta, ta sa duniya da mazaunanta su yi wa dabba ta farin nan sujada, wadda
aka warkar mata da raunin nan da zai iya kashe ta. 13 Ta kuma yi manyan ayyuka
da kuma alamu masu banmamaki, har ta sa wuta ta sauko daga sama zuwa ƙasa a
gaban idon mutane. 14 Saboda alamun nan da aka ba ta iko tă yi a madadin dabban
nan ta fari, sai ta ruɗi mazaunan duniya. Ta umarce su su kafa siffa don girmama
dabbar da aka ji mata rauni da takobi duk da haka ta rayu. 15 Aka ba ta iko tă ba
da numfashi ga siffar dabban nan ta fari, don tă yi magana tă kuma sa a kashe duk
waɗanda suka ƙi yi wa siffar sujada. 16 Ta kuma tilasta wa kowa, manya da yara,
mawadata da matalauta, 'yantattu da bayi, don a yi musu alama a hannun dama ko
a goshi, 17 don kada kowa yă saya ko yă sayar, sai dai yana da alamar, wadda take
sunan dabbar ko kuma lambar sunanta.
18 Wannan yana bukata hikima. Duk mai hankali, sai yă lissafta lambar dabbar,
gama lamban nan ta mutum ne. Lambarta kuwa ita ce 666.

# 14

### *Ɗan Ragon da 144,000*

1 Sai na duba, can a gabana kuwa ga Ɗan Rago, tsaye a kan Dutsen Sihiyona, tare da
shi akwai kuma mutane 144,000 waɗanda suke da sunansa da sunan Ubansa a rubuce
a goshinsu. 2 Sai na ji ƙara daga sama kamar motsin ruwaye masu gudu, kamar kuma
tsawa. Karar da na ji ta yi kamar ta masu garaya da suke kiɗin garayarsu. 3 Suka
kuwa rera sabuwar waƙa a gaban kursiyin da kuma a gaban halittu huɗun nan
masu rai, da kuma a gaban dattawa. Ba wanda ya iya koyon waƙar sai mutanen nan
144,000 da aka fansa daga duniya. 4 Waɗannan su ne waɗanda ba su ƙazantar da
kansu da mata ba, gama sun kiyaye kansu da tsarki. Suna bin Ɗan Ragon duk inda
ya tafi. Su ne aka saya daga cikin mutane aka kuwa miƙa su kamar 'ya'yan fari ga
Allah da kuma Ɗan Ragon. 5 Ba a sami ƙarya a bakunansu ba; su kuma marasa aibi
ne.

### *Mala'iku uku*

6 Sai na ga wani mala'ika yana tashi sama a tsakiyar sararin sama, yana kuma
da madawwamiyar bishara wadda zai yi shela ga waɗanda suke zama a duniya, ga
kowace al'umma, kabila, harshe, da kuma jama'a. 7 Ya ce da babbar murya, "Ku ji
tsoron Allah ku kuma ɗaukaka shi, domin sa'ar hukuncinsa ya yi. Ku yi wa wannan
da ya halicci sammai, ƙasa, teku, da maɓulɓulan ruwa sujada."
8 Mala'ika na biyu ya biyo yana cewa, "Ta fāɗi! Babilon Mai Girma ta fāɗi, wadda
ta sa dukan al'ummai suka sha ruwan inabin hauka na zinanta."
9 Mala'ika na uku ya biyo su ya ce da babbar murya, "Duk wanda ya yi wa dabban
nan da siffarta sujada ya kuma sami alamarta a goshi ko a hannu, 10 shi ma zai sha
ruwan inabin fushin Allah, wanda aka zuba da duk ƙarfinsa a kwaf fushinsa. Za
a ba shi azaba da farar wuta mai ci a gaban tsarkakan mala'iku da na Ɗan Ragon.
11 Hayaƙin azabarsu kuwa zai dinga tashi har abada abadin. Kuma babu hutu dare
ko rana wa waɗanda suke wa dabbar da siffarta sujada, ko kuwa ga duk wanda ya
sami alamar sunanta." 12 Wannan yana bukata haƙuri, a gefen tsarkakan da suke
biyayya da umarnan Allah suka kuma kasance da aminci ga Yesu.
13 Sai na ji murya daga sama ta ce, "Rubuta, Masu albarka ne matattun da suka
mutu cikin Ubangiji daga yanzu zuwa gaba."
"I, za su huta daga faman aikinsu, gama ayyukansu za su bi su," in ji Ruhu.

### *Girbin duniya*

[14] Na duba, can gabana kuwa ga farin girgije, zaune kuma a kan girgijen kuwa ga
wani da ya yi kamar “ɗan mutum”* tare da rawanin zinariya a kansa da kuma lauje
mai kaifi a hannunsa. [15] Sai wani mala’ika ya fito daga haikali ya kuma yi kira da
babbar murya ga wannan mai zaune a kan girgijen ya ce, “Dauki laujenka ka yi girbi,
domin lokacin girbi ya yi, gama amfanin da yake duniya ya nuna.” [16] Sai wannan
mai zaune a girgijen ya wurga laujensa a duniya, sai aka kuwa girbe duniya.
[17] Wani mala’ika kuma ya fito daga haikali a sama, shi ma yana da lauje mai kaifi.
[18] Har yanzu, wani mala’ika mai lura da wuta, ya fito daga bagaden ya yi kira da
babbar murya ga wannan wanda yake da lauje mai kaifi ya ce, “Ɗauki laujenka mai
kaifi ka tattara kawunan ’ya’yan inabi daga kuringar inabin duniya, domin ’ya’yan
inabin sun nuna.” [19] Mala’ikan ya wurga laujensa a duniya, ya tattara ’ya’yan inabin,
ya kuma zuba su cikin babbar wurin matsewar inabin fushin Allah. [20] Aka tattake
su a wurin matsin inabi a bayan gari, jini kuwa ya yi ta gudana daga wurin matsin
inabi tsayinsa ya kai kamar tsawon linzami a bakin doki, nisansa kuma ya kai wajen
kilomita 300.

# 15

*Mala’iku bakwai da annobai bakwai*

[1] Na ga wata babbar alama mai banmamaki a sama, mala’iku bakwai da annobai
bakwai na ƙarshe, na ƙarshe, domin da su ne fushin Allah ya cika. [2] Sai na ga abin da
ya yi kamar tekun gilashi gauraye da wuta kuma tsaye kusa da teku, waɗanda suka
ci nasara bisan dabbar da siffarta da bisan lambar sunanta. Suna riƙe da garayu
waɗanda Allah ya ba su [3] suka rera waƙar Musa bawan Allah da kuma waƙar Ɗan
Ragon suna cewa,

“Ayyukanka suna da girma da kuma banmamaki,
ya Ubangiji Maɗaukaki.
Al’amuranka suna da aminci da kuma gaskiya,
ya Sarkin zamanai.
[4] Wane ne ba zai ji tsoronka,
yǎ kuma kawo ɗaukaka ga sunanka ba, ya Ubangiji?
Gama kai kaɗai ne mai tsarki.
Dukan al’ummai za su zo
su yi sujada a gabanka,
gama an bayyana ayyukan adalcinka.”

[5] Bayan wannan sai na duba, a cikin sama kuwa sai ga haikali, wato, tabanakul
na Shaida, a buɗe. [6] Daga cikin haikalin mala’iku bakwai tare da annobai bakwai
suka fito. Suna saye da tufafin lilin masu tsabta masu walƙiya, suna kuma saye da
ɗamarar zinariya a ƙirjinsu. [7] Sai ɗaya daga cikin halittu huɗun nan masu rai, ya
ba wa mala’iku bakwai nan kwanonin zinariya bakwai cike da fushin Allah, wanda
yake raye har abada abadin. [8] Aka kuma cika haikalin da hayaƙi daga ɗaukakar Allah
da kuma daga ikonsa, kuma ba wanda ya iya shiga haikalin sai da aka cika annobai
bakwai nan na mala’iku bakwai.

# 16

*Kwanoni bakwai na fushin Allah*

[1] Sai na ji wata babbar murya daga haikalin tana ce wa mala’iku bakwai nan, “Ku
tafi ku zuba kwanoni bakwai nan na fushin Allah a kan duniya.”

* **14:14** Dubi Dan 7.13.

2 Mala'ika na fari ya je ya juye kwanonsa a bisan ƙasa, sai munanan gyambuna
masu zafi suka fito a jikin mutanen da suke da alamar dabbar suka kuma yi wa
siffarta sujada.

3 Mala'ika na biyu ya juye kwanonsa a bisan teku, sai tekun ya zama jini kamar na
mataccen mutum, kuma kowane abu mai rai da yake cikin tekun ya mutu.

4 Mala'ika na uku ya juye kwanonsa a bisan koguna da maɓulɓulan ruwa, sai suka
zama jini. 5 Sa'an nan na ji mala'ikan da yake lura da ruwaye ya ce,

"Kai mai adalci ne cikin waɗannan hukuntai,
kai da kake yanzu, kake kuma a dā, Mai Tsarki, saboda yadda ka yi hukuncin nan;
6 gama sun zub da jinin tsarkakanka da kuma annabawanka,
ka kuwa ba su jini su sha, yadda ya dace da su."
7 Na kuma ji bagaden ya amsa,
"I, Ubangiji Allah, Maɗaukaki,
hukuntanka daidai yake na adalci ne kuma."

8 Mala'ika na huɗu ya juye kwanonsa a bisan rana, sai aka ba wa rana iko ta ƙona
mutane da wuta. 9 Aka ƙone su da zafin wuta mai tsanani suka kuwa la'anci sunan
Allah wanda yake da iko a kan waɗannan annoban, amma suka ƙi su tuba su kuma
ɗaukaka shi.

10 Mala'ika na biyar ya juye kwanonsa a bisan gadon sarautar dabbar, mulkinta
kuwa ya zama duhu. Mutane suka yi ta cizon bakinsu saboda azaba 11 suka kuma
la'anci Allah na sama saboda zafinsu, da kuma saboda gyambunansu, amma suka ƙi
su tuba daga abin da suka riga suka yi.

12 Mala'ika na shida ya juye kwanonsa a bisan babban kogin Yuferites, sai ruwansa
ya shanye don a shirya hanya saboda sarakuna daga Gabas. 13 Sa'an nan na ga
mugayen ruhohi guda uku da suka yi kamar kwaɗi; suka fito daga bakin macijin
nan, da kuma daga bakin dabbar, da kuma daga bakin annabin ƙaryan nan. 14 Su
ruhohin aljanu ne da suke aikata abubuwan banmamaki, sukan je wurin sarakunan
dukan duniya, don su tattara su don yaƙi a babbar ranar Allah Maɗaukaki.

15 "Ga shi, ina zuwa kamar ɓarawo! Mai albarka ne wanda yake zama a faɗake
yana kuma saye da tufafinsa, don kada yă yi tafiya tsirara a kuma kunyata shi."

16 Sa'an nan aka tattara sarakuna zuwa wurin da a Ibraniyanci ake kira Armageddon.

17 Mala'ika na bakwai ya juye kwanonsa cikin iska, daga haikalin kuwa sai aka
ji wata babbar murya daga kursiyin, tana cewa, "An gama!" 18 Sai ga walƙiya,
ƙararraki, tsawa da kuma matsananciyar girgizar ƙasa. Ba a taɓa yin irin
wannan girgizar ƙasar ba, tun kasancewar mutum a duniya, girgizar ƙasar kuwa
gawurtacciya ce. 19 Babban birnin ya rabu kashi uku, biranen al'ummai kuma suka
rurrushe. Allah ya tuna da Babilon Mai Girma ya kuma ba ta kwaf cike da ruwan
inabin fushinsa. 20 Kowane tsibiri ya gudu ba a kuwa ƙara ganin duwatsu ba. 21 Daga
sararin sama manyan ƙanƙara masu nauyin gaske suka fāɗo a kan mutane. Suka
kuma la'anci Allah saboda annobar ƙanƙarar, domin annobar ta yi muni ƙwarai.

# 17

*Babilon, karuwa a kan dabbar*

1 Ɗaya daga cikin mala'iku bakwai masu ɗauke da kwanoni bakwai nan, ya zo ya
ce mini, "Zo, zan nuna maka hukuncin babbar karuwan nan da take zaune a bisan
ruwaye masu yawa. 2 Da ita ce sarakunan duniya suka yi zina mazaunan duniya
kuma suka bugu da ruwan inabin zinace zinacenta."

3 Sa'an nan mala'ikan ya ɗauke ni cikin Ruhu zuwa hamada. A can na ga mace
zaune a kan wata jan dabbar da aka rufe da sunayen saɓo tana kuma da kawuna
bakwai da ƙahoni goma. 4 Macen tana saye da tufafi masu ruwan ja da shunayya,
tana ƙyalli da zinariya, duwatsu masu daraja da kuma lu'ulu'ai. Tana riƙe da kwaf
na zinariya a hannunta, cike da abubuwa masu banƙyama da kuma ƙazantar zinace
zinacenta. 5 Sunan da aka rubuta a goshinta asiri ne,

Babilon mai girma
mahaifiyar karuwai
da kuma na abubuwa masu banƙyama na duniya.

6 Na ga cewa macen ta bugu da jinin tsarkaka, jinin waɗanda suka shaida Yesu.
Da na gan ta, sai na yi mamaki ƙwarai. 7 Sa'an nan mala'ikan ya ce mini, "Don
me kake mamaki? Zan bayyana maka asirin macen nan da dabbar da take hawa,
wadda take da kawuna bakwai da ƙahoni goma. 8 Dabbar da ka gani, a dā ta taɓa
kasancewa, a yanzu, ba ta, za tă kuma fito daga Abis zuwa ga hallakarta. Mazaunan
duniya waɗanda ba a rubuta sunayensu a littafin rai tun kafin halittar duniya ba za
su yi mamaki sa'ad da suka ga dabbar, domin a dā ta taɓa kasancewa, yanzu kuwa
ba ta, duk da haka za tă dawo.

9 "Wannan yana bukata hankali da kuma hikima. Kawuna bakwai nan tuddai
bakwai ne da macen take zama a kai. 10 Sarakuna bakwai ne kuma. Biyar sun fāɗi,
ɗaya yana nan, ɗayan kuma bai zo ba tukuna; amma sa'ad da ya zo, zai kasance na
ɗan lokaci. 11 Dabbar da a dā ta taɓa kasancewa, amma yanzu ba ta, ita ce sarki na
takwas. Ita ɗaya ce cikin bakwai ɗin, kuma tana tafiya zuwa ga hallakarta.

12 "Kahonin nan goma da ka gani sarakuna goma ne da ba su riga sun karɓi mulki
ba, amma waɗanda na sa'a guda za su karɓi iko a matsayin sarakuna tare da dabbar.
13 Suna da manufa guda za su kuma ba wa dabbar ikonsu da kuma sarautarsu. 14 Za
su yi yaƙi da Ɗan Ragon, sai dai Ɗan Ragon zai ci nasara a bisansu domin shi ne
Ubangijin iyayengiji, Sarkin sarakuna, tare da shi kuwa kirayayunsa, zaɓaɓɓunsa da
kuma amintattu masu binsa za su kasance."

15 Sa'an nan mala'ikan ya ce mini, "Ruwayen da ka gani, inda karuwan take zama,
jama'a ce, taro masu yawa, al'ummai da kuma harsuna. 16 Dabbar da kuma ƙahoni
goma da ka gani za su ƙi jinin karuwar. Za su kai ta ga hallaka su kuma bar ta
tsirara; za su ci namanta su kuma ƙone ta da wuta. 17 Gama Allah ya sa a zukatansu
su cika nufinsa ta wurin yarda su ba wa dabbar ikonsu tă yi mulki, sai lokacin da
kalmomin Allah sun cika. 18 Macen da ka gani ita ce babban birnin da yake mulki a
bisan sarakunan duniya."

# 18

*Makoki a kan Babilon*

1 Bayan wannan sai na ga wani mala'ika yana saukowa daga sama. Yana da iko
mai girma, aka haskaka duniya da darajarsa. 2 Ya yi kira da babbar murya ya ce,

"Ta fāɗi! Babilon Mai Girma ta fāɗi.
Ta zama gidan aljanu
da kuma wurin zaman kowace irin mugun ruhu,
wurin zaman kowane irin tsuntsu marar tsabta da mai banƙyama.
3 Gama dukan al'ummai sun sha ruwan inabin
haukan zinace zinacenta.
Sarakunan duniya sun yi zina tare da ita,
attajiran duniya kuma sun arzuta da almubazzarancinta."

4 Sai na ji wata murya daga sama ta ce,

"Ku fita daga cikinta, mutanena,
don kada zunubanta su shafe ku,

don kada wata annobarta ta same ku;
5 gama zunubanta sun yi tsororuwa sun kai sama.
Allah kuma ya tuna da laifofinta.
6 Ku sāka mata kamar yadda ta sāka muku;
ku sāka mata sau biyu na abin da ta yi.
Ku dama mata sau biyu na abin da yake cikin kwaf nata.
7 Ku ba ta isashen azaba da baƙin ciki
kamar daraja da kuma jin daɗin da ta ba wa kanta.
A zuciyarta takan yi taƙama, ta ce,
'Ina zama kamar sarauniya;
ni ba gwauruwa ba ce,
kuma ba zan taɓa yin makoki ba.'
8 Saboda haka a rana ɗaya annobarta za su cim mata,
mutuwa, makoki da kuma yunwa.
Wuta zai cinye ta,
gama Ubangiji Allah mai girma ne, wanda yake shari'anta ta.
9 "Sa'ad da sarakunan duniya da suka yi zina da ita suka kuma yi tarayya cikin jin
daɗinta suka ga hayaƙin ƙunarta, za su yi kuka da makoki saboda ita. 10 Don tsoron
ganin azabarta za su tsaya daga nesa, su yi kuka suna cewa,
" 'Kaito! Kaito, ya birni mai girma.
Ya ke Babilon, birni mai iko!
Cikin sa'a guda hallakarki ta zo!'
11 "Attajiran duniya za su yi kuka su kuma yi makoki a kanta, domin ba wanda
yake ƙara sayen kayayyakinsu 12 kayayyakin zinariya, azurfa, duwatsu masu daraja
da lu'ulu'ai; lallausan lilin, tufa masu ruwan shunayya, siliki da jan tufa; da kowane
irin katakai masu ƙanshi da kayayyaki na kowane iri da aka yi da hauren giwa,
katakai masu tsada, tagulla, baƙin ƙarfe da dutse mai sheƙi; 13 kayayyakin sinnamon
da kayan yaji, na turaren wuta, mur da turare, na ruwan inabi da man zaitun, na
gari mai laushi da alkama; shanu da tumaki; dawakai da kekunan doki, da jikuna da
kuma rayukan mutane.
14 "Za su ce, 'Amfanin da kike marmari ya kuɓuce. Dukan arzikinki da darajarki
sun ɓace, ba kuwa za a ƙara samunsu ba.' 15 Attajiran da suka sayar da waɗannan
kayayyaki suka kuma sami arzikinsu daga gare ta za su tsaya daga nesa, cike da
tsoron ganin azabarta. Za su yi kuka da makoki 16 su ce,
" 'Kaito! Kaito, ya birni mai girma,
saye da lallausan lilin, shunayya da kuma ja,
mai walƙiya da zinariya, duwatsu masu daraja da kuma lu'ulu'ai!
17 Cikin sa'a guda irin wannan dukiya mai yawa ta hallaka!'
"Duk matuƙan jirgin ruwa, da dukan waɗanda suke tafiya a jirgin ruwa,
ma'aikatanta, da duk masu samun abin zama gari daga teku za su tsaya daga nesa.
18 Sa'ad da suka ga hayaƙin ƙunarta, za su yi ihu su ce, 'An taɓa samun birni kamar
wannan babban birnin kuwa?' 19 Za su zuba ƙura a kawunansu, da kuka da makoki
za su yi ta kururuwa,
" 'Kaito! Kaito, ya birni mai girma,
inda dukan waɗanda suke da jiragen ruwa a teku
suka arzuta da ɗumbun dukiyarsa!
Cikin sa'a ɗaya ta hallaka!'

20 "Ki yi murna a kanta, ya sama!
Ku yi murna, ku tsarkaka!

Ku yi murna, ku manzanni da annabawa!
Allah ya hukunta shi
saboda abin da ya yi muku."
21 Sa'an nan wani mala'ika mai ƙarfi ya ɗauki dutse kamar girman babban dutsen
niƙa ya jefa cikin teku ya ce,
"Da wannan irin giggitawa
za a jefar da birnin Babilon mai girma ƙasa,
ba za a ƙara ganin ta ba.
22 Ba za a ƙara jin
ƙarar kiɗin masu garaya da muryar mawaƙa, da na masu bushe-bushe, da na masu busan ƙaho
a cikinki ba.
Ba za a ƙara samun ma'aikaci na kowace irin sana'a
a cikinki kuma ba.
Ba za a ƙara jin ƙarar dutsen niƙa
a cikinki kuma ba.
23 Hasken fitila ba zai ƙara haskakawa
a cikinki ba.
Ba za a ƙara jin muryar ango da amarya
a cikinki ba.
Attajiranki, dā su ne manyan mutanen duniya.
Ta wurin sihirinki, dukan ƙasashe sun kauce.
24 A cikinta aka sami jinin annabawa, da na tsarkaka,
da kuma na dukan waɗanda aka kashe a duniya."

# 19

*Halleluya sau uku a kan fāɗuwar Babilon*

1 Bayan wannan sai na ji abin da ya yi kamar ƙasaitaccen taron mutane a sama,
suna cewa,
"Halleluya!
Ceto da ɗaukaka da iko sun tabbata ga Allahnmu,
2 gama hukuncinsa daidai ne, mai adalci kuma.
Ya hukunta babbar karuwan nan
wadda ta ɓata duniya da zinace zinacenta.
Ya rama jinin bayinsa a kanta."
3 Suka sāke tā da murya suka ce,
"Halleluya!
Hayaƙin yake fitowa daga wurinta ya yi ta tashi sama har abada abadin."
4 Dattawan nan ashirin da huɗu da halittu huɗun nan masu rai suka fāɗi suka yi
wa Allah sujada, wannan da yake zaune a kursiyi. Suka tā da murya suka ce,
"Amin, Halleluya!"
5 Sa'an nan wata murya ta fito daga kursiyin, tana cewa,
"Ku yabi Allahnmu,
dukanku da kuke bayinsa,
ku da kuke tsoronsa,
babba da yaro!"
6 Sai na ji wani abu mai ƙara kamar ƙasaitaccen taron mutane, kamar rurin
ruwaye masu gudu da kuma kamar bugun tsawa mai ƙarfi, suna tā da murya suna
cewa,
"Halleluya!
Gama Ubangiji Allahnmu Maɗaukaki ne yake mulki.
7 Bari mu yi farin ciki mu kuma yi murna

mu kuma ɗaukaka shi!
Domin lokacin auren Ɗan Ragon ya yi,
amaryarsa kuwa ta shirya kanta.
8 Aka ba ta lallausan lilin, mai haske da tsabta
ta sanya."
(Lallausan lilin yana misalta ayyukan adalci na tsarkaka.)

9 Sai mala'ikan ya ce mini, "Rubuta, 'Masu albarka ne waɗanda aka gayyace su
zuwa bikin auren Ɗan Ragon!' " Sai ya ƙara da cewa, "Waɗannan su ne kalmomin
Allah da gaske."
10 Da wannan sai na fāɗi a gabansa, don in yi masa sujada. Amma ya ce mini,
"Kada ka yi haka! Ni ma abokin bauta ne da kai da kuma 'yan'uwanka waɗanda
suke riƙe da shaidar Yesu. Ka yi wa Allah sujada! Domin shaidar Yesu ita ce ruhun
annabci."

### *Mahayi a kan farin doki*

11 Sai na ga sama a buɗe can kuwa a gabana ga farin doki, sunan mahayinsa Mai
Aminci da Mai Gaskiya ne. Da adalci yake shari'a yake kuma yaƙi. 12 Idanunsa sun yi
kamar harshen wuta, a kansa kuwa akwai rawani masu yawa. Yana da suna rubuce
a kansa da babu wanda ya sani sai dai shi. 13 Yana saye da rigar da aka tsoma a
jini, sunansa kuwa Kalman Allah ne. 14 Mayaƙan sama suna biye da shi, suna hawan
fararen dawakai, saye da fararen tufafi masu tsabta na lallausan lilin. 15 Daga bakinsa
takobi mai kaifi ya fito. Da shi zai karkashe al'ummai. "Zai yi mulkinsu da sandan
sarautar ƙarfe." Yana tattake wurin matsin ruwan inabi na fushin Allah Maɗaukaki.
16 A rigarsa da kuma a cinyarsa akwai wannan suna a rubuce,
Sarkin sarakuna da Ubangijin iyayengiji.
17 Na kuma ga wani mala'ika tsaye a cikin rana, wanda ya yi kira da babbar murya
ga dukan tsuntsaye da suke tashi sama a tsakiyar sararin sama cewa, "Ku zo, ku
taru don babban bikin nan na Allah, 18 don ku ci naman sarakuna, jarumawa, da
kuma manyan mutane, na dawakai da mahayansu, da kuma naman dukan mutane,
'yantacce da bawa, babba da yaro."
19 Sa'an nan na ga dabbar da sarakunan duniya da mayaƙansu sun taru don su
yi yaƙi da wannan wanda yake kan farin dokin da kuma mayaƙansa. 20 Amma aka
kama dabbar tare da annabin ƙaryan nan wanda ya aikata alamu masu banmamaki
a madadinta. Da waɗannan alamun ne ya ruɗe waɗanda suka sami alamar dabbar
suka kuma bauta wa siffarta. Aka jefa dukansu biyu da rai cikin tafkin wuta ta da
farar wuta mai ci. 21 Sauran kuma aka kashe su da takobin da ya fito daga bakin
wannan wanda yake kan dokin. Dukan tsuntsaye kuwa suka ci namansu iyakar
iyawarsu.

## 20

### *Shekaru dubu*

1 Na kuma ga wani mala'ika yana saukowa daga sama, yana da mabuɗin Abis yana
kuma riƙe da ƙaton sarƙa a hannunsa. 2 Ya kama macijin, wannan tsohon maciji,
wanda yake shi ne Iblis, ko kuwa Shaiɗan, aka kuma ɗaura shi har shekara dubu.
3 Ya jefa shi cikin Abis, ya kuma kulle ya sa hatimi a kansa, don a hana kada yǎ ƙara
ruɗin al'ummai, sai shekarun nan dubu sun cika. Bayan wannan, dole a sake shi na
ɗan lokaci.
4 Na ga kursiyoyi inda waɗanda aka ba su ikon shari'a suke zama a kai. Sai na ga
rayukan waɗanda aka yanke kawunansu saboda shaidarsu don Yesu saboda kuma
maganar Allah. Ba su yi wa dabban nan ko siffarta sujada ba, ba su kuma sami

alamarta a goshinsu ko a hannuwansu ba. Suka sāke rayuwa daga matattu, suka yi
mulki tare da Kiristi shekaru dubu. 5 (Sauran matattu ba su sāke rayuwa ba, sai da
shekaru dubun nan suka cika.) Wannan fa shi ne tashin matattu na farko. 6 Masu
albarka da kuma tsarki ne waɗanda suke da rabo a tashin matattu na farko. Mutuwa
ta biyu ba ta da iko a kansu, sai dai za su zama firistocin Allah da kuma na Kiristi za
su kuma yi mulki tare da shi na shekaru dubu.

*Hallakar Shaiɗan*

7 Sa'ad da shekaru dubun nan suka cika, za a saki Shaiɗan daga kurkukun da yake,
8 zai kuma fito don yă ruɗi al'ummai da suke a kursuyoyi huɗu na duniya, Gog da
Magog, yă tattara su don yaƙi. Yawansu kuwa ya yi kamar yashi a bakin teku. 9 Suka
mamaye duk fāɗin duniya suka kuma kewaye sansanin mutanen Allah, birnin da
yake ƙauna. Amma wuta ta fito daga sama ta cinye su. 10 Aka jefa Iblis da ya ruɗe
su cikin tafkin farar wuta, inda aka jefa dabban nan da annabin ƙaryan nan. Za a
ba su azaba dare da rana har abada abadin.

*An shari'anta matattu*

11 Sa'an nan na ga babban farin kursiyi da kuma wannan da yake zama a kansa.
Duniya da sararin sama kuwa suka ɓace daga gabansa, babu wuri kuwa dominsu.
12 Sai na ga matattu, babba da yaro tsaye a gaban kursiyin, aka kuma buɗe littattafai.
Aka buɗe wani littafi, wanda yake shi ne littafin rai. Aka yi wa matattu shari'a bisa ga
abin da suka aikata yadda yake a rubuce a cikin littattafai. 13 Teku ya ba da matattu
da suke cikinsa, mutuwa da Hades kuma suka ba da matattu da suke cikinsu, aka
kuma yi wa kowane mutum shari'a bisa ga abin da ya aikata. 14 Sa'an nan aka jefar
da mutuwa da kuma Hades cikin tafkin wuta. Tafkin wutar nan kuwa shi ne mutuwa
ta biyu. 15 Duk wanda ba a sami sunansa a rubuce a cikin littafin rai ba, an jefar da
shi cikin tafkin wutar nan.

# 21

*Sabuwar sama da sabuwar duniya*

1 Sa'an nan na ga sabon sama da sabuwar duniya, gama sama na farko da duniya ta
farko sun shuɗe, babu kuma wani teku. 2 Na ga Birni Mai Tsarki, sabuwar Urushalima
tana saukowa daga sama, daga Allah, a shirye kamar amaryar da aka yi mata ado
mai kyau saboda mijinta. 3 Na kuma ji wata babbar murya daga kursiyin tana cewa,
"Yanzu mazaunin Allah yana tare da mutane, zai kuma zauna tare da su. Za su zama
mutanensa, Allah kansa kuwa zai kasance tare da su yă kuma zama Allahnsu. 4 Zai
share dukan hawaye daga idanunsu. Ba sauran mutuwa ko makoki ko kuka ko azaba,
gama tsofaffin al'amura sun shuɗe."

5 Wannan da yake zaune a kursiyin ya ce. "Ina yin kome sabo!" Sai ya ce, "Rubuta
wannan, domin waɗannan kalmomi amintattu ne gaskiya ne kuma."

6 Ya ce mini, "An gama. Ni ne Alfa da kuma Omega, na Farko da kuma na Karshe.
Duk mai jin ƙishirwa zan ba shi abin sha kyauta daga maɓulɓular ruwan rai. 7 Duk
wanda ya ci nasara zai gāji dukan wannan, zan kuma zama Allahnsa, shi kuma zai
zama ɗana. 8 Amma matsorata, da marasa bangaskiya, masu ƙazanta, masu kisankai,
masu fasikanci, masu sihiri, masu bautar gumaka da dukan maƙaryata, wurinsu zai
kasance a cikin tafkin wutar da yake farar wuta mai ci. Wannan fa ita ce mutuwa ta
biyu."

9 Ɗaya daga cikin mala'ikun nan bakwai masu kwanonin nan bakwai cike da
annoban nan bakwai na ƙarshe, ya zo ya ce mini "Zo, zan nuna maka amaryar,
matar Ɗan Ragon." 10 Ya kuwa ɗauke ni cikin Ruhu zuwa wani babban dutse mai
tsayi, ya kuma nuna mini Birni Mai Tsarki, Urushalima, tana saukowa daga sama,
daga Allah. 11 Ya haskaka da ɗaukakar Allah, haskensa kuwa ya yi kamar lu'ulu'u

mai daraja sosai, kamar yasfa, yana ƙyalƙyali kamar madubi. 12 Yana da babbar
katanga mai tsayi, mai ƙofofi goma sha biyu, da kuma mala’iku goma sha biyu a
ƙofofin. A bisa ƙofofin an rubuta sunayen kabilu goma sha biyu na Isra’ila. 13 Akwai
ƙofofi uku a gabas, uku a arewa, uku a kudu, uku kuma a yamma. 14 An gina katangar
birnin a kan tushen gini goma sha biyu, a kansu kuwa akwai sunayen manzannin
sha biyu na Ɗan Ragon.

15 Mala’ikan da ya yi magana da ni yana da sandan awo na zinariya don awon
birnin, ƙofofinsa, da kuma katangarsa. 16 Birnin murabba’i ne, tsayinsa daidai ne da
fāɗinsa. Ya auna birnin da sandarsa ya kuwa sami mil 1,400 (wajen kilomita 2,200)
tsawonsa, fāɗinsa da kuma tsayinsa daidai suke. 17 Ya auna katangarsa ya kuma sami
ƙaurinta kamun 144, bisa ga ma’aunin mutum, wanda mala’ikan ya yi amfani da shi.
18 An yi katangar da yasfa, birnin kuma da zinariya zalla, yana kuma ƙyalli kamar
madubi. 19 Tushen ginin katangar birnin kuwa an yi masa adon da kowane irin dutse
mai daraja. Tushe na farko an yi shi yasfa, na biyu saffaya, na uku agat, na huɗu
zumurrudu, 20 na biyar onis, na shida yakutu, na bakwai kirisolit, na takwas beril,
na tara tofaz, na goma kirisofuras, na goma sha ɗaya yasin, na goma sha biyu kuma
ametis. 21 Kofofi goma sha biyun nan lu’ulu’ai goma sha biyu ne, kowace ƙofa an yi
ta da lu’ulu’u guda. Babban titin birnin kuwa an yi shi da zinariya zalla, yana kuma
ƙyalli kamar madubi.

22 Ban ga haikali a cikin birnin ba, domin Ubangiji Allah Maɗaukaki da kuma Ɗan
Ragon ne haikalin birnin. 23 Birnin ba ya bukatar rana ko wata su haskaka shi, gama
ɗaukakar Allah tana ba shi haske, Ɗan Ragon kuwa shi ne fitilar birnin. 24 Al’ummai
za su yi tafiya cikin hasken birnin, sarakunan duniya kuma za su kawo darajarsu
cikin birnin. 25 Ba za a taɓa rufe ƙofofin birnin da rana ba, gama ba za a yi dare a
can ba. 26 Za a kawo ɗaukaka da girmar al’ummai a cikin birnin. 27 Babu wani abu
marar tsarkin da zai taɓa shiga cikin birnin, babu kuma wani mai aikata abin kunya
ko ruɗi da zai shiga, sai dai waɗanda aka rubuta sunayensu a cikin littafin rai na
Ɗan Ragon.

# 22

*An maido da Eden*

1 Sai mala’ikan ya nuna mini kogin ruwan rai, mai ƙyalli kamar madubi, yana
gangarawa daga kursiyin Allah da na Ɗan Ragon, 2 yana bin tsakiyar babban titi na
birnin. A kowane gefen kogin akwai itacen rai mai ba da ’ya’ya goma sha biyu, yana
ba da ’ya’yansa kowane wata. Ganyayen itacen kuwa saboda warkar da al’ummai
ne. 3 Ba za a ƙara samun la’ana ba. Kursiyin Allah da na Ɗan Ragon zai kasance a
cikin birnin, bayinsa kuma za su yi masa hidima. 4 Za su ga fuskarsa, sunansa kuma
zai kasance a goshinsu. 5 Ba za a ƙara yin dare ba. Ba za su bukaci hasken fitila ko
hasken rana ba, domin Ubangiji Allah zai haskaka su. Za su kuwa yi mulki har abada
abadin.

*Yohanna da Mala’ikan*

6 Mala’ikan ya ce mini, “Waɗannan kalmomi amintattu ne gaskiya ne kuma.
Ubangiji, Allahn ruhohin annabawa, ya aiki mala’ikansa, don yǎ nuna wa bayinsa
abubuwan da za su faru nan ba da daɗewa ba.”

7 “Ga shi! Ina zuwa da wuri! Mai albarka ne wanda yake kiyaye kalmomin
annabcin da suke cikin wannan littafi.”

8 Ni, Yohanna, na ji, na kuma ga abubuwan nan. Kuma sa’ad da na ji, na kuma
gan su, sai na fāɗi a ƙasa a gaban mala’ikan da yake nuna mini su, don in yi sujada.

9 Amma ya ce mini, "Kada ka yi haka! Ni abokin bautarku ne, kai da 'yan'uwanka
annabawa, da kuma waɗanda suke kiyaye kalmomin wannan littafi. Allah za ka yi
wa sujada!"
10 Sa'an nan ya gaya mini cewa, "Kada ka rufe kalmomin annabcin littafin nan,
domin lokaci ya yi kusa. 11 Duk mai yin laifi yă ci gaba da yin laifi; duk mai aikata
ƙazanta yă ci gaba da aikata ƙazanta. Duk mai aikata abin da yake daidai, yă ci gaba
da aikata abin da yake daidai. Kuma duk wanda yake mai tsarki, yă ci gaba da yin
abin da yake da tsarki."

*Maganar ƙarshe. Gayyata da gargaɗi*

12 "Ga shi, ina zuwa da wuri! Ladan da zan bayar yana tare da ni, kuma zan ba wa
kowa gwargwadon abin da ya yi. 13 Ni ne Alfa da kuma Omega, na Fari da kuma na
Baya, Farko da kuma Karshe.

14 "Masu albarka ne waɗanda suka wanke tufafinsu, don su sami izinin ci daga
itacen rai su kuma shiga birnin ta ƙofofi. 15 Waɗanda suke waje kuwa karnuka ne,
masu sihiri, masu fasikanci, masu kisankai, masu bautar gumaka, da duk wanda yake
ƙaunar ƙarya yake kuma aikata ta.

16 "Ni, Yesu, na aiko mala'ikana ya ba ka wannan shaida saboda ikkilisiyoyi. Ni ne
Tushe da kuma Zuriyar Dawuda, da kuma Taurarон Asubahi mai haske."

17 Ruhu da kuma amarya suna cewa, "Zo!" Duk wanda ya ji kuwa, yă ce, "Zo!" Duk
mai jin ƙishirwa, yă zo; duk mai bukata kuma, yă ɗibi ruwan rai kyauta.

18 Ina yin wa duk wanda ya ji kalmomin annabcin wannan littafi gargaɗi. Duk
wanda ya ƙara wani abu a kansu, Allah zai ƙara masa annoban da aka bayyana a
littafin nan. 19 Duk wanda kuma ya yi ragi a kalmomi daga littafin annabcin nan,
Allah zai ɗauke rabonsa na itacen rai da kuma na birnin nan mai tsarki, waɗanda
aka bayyana a littafin nan.

20 Shi da ya shaida waɗannan abubuwa ya ce, "I, ina zuwa da wuri."
Amin. Zo, Ubangiji Yesu!

21 Alherin Ubangiji Yesu yă kasance tare da mutanen Allah. Amin.